
القرآن الكريم

وترجمة معانيه إلى لغة الهوسا



جمعية الدعوة الإسلامية العالمية

طرابلس - الجماهيرية العربية الليبية الشعبية الاشتراكية العظمى

القرآن الكريم

وترجمة معانيه إلى لغة الهوسا

Al-Ḱur-Ani Mai Girma

Da Fassarar Ma-Anarsa
Zuwa Harshen Hausa



جمعية الدعوة الإسلامية العالمية
طرابلس - الجماهيرية العربية الليبية الشعبية الاشتراكية العظمى
Ḱungiyar Kira Zuwaga Musulunci ta Duniya
Tripoli - Jamahiriyar Larabawan Libiya
Ta Yan Ḱasa Ta Tarayya Mai Girma

1 سُورَةُ الفَاتِحَةِ مَكِّيَّة
وآياتها سبع 7

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ 1 ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ 2
مَٰلِكِ يَوْمِ ٱلدِّينِ 3 إِيَّاكَ نَعْبُدُ وَإِيَّاكَ
نَسْتَعِينُ 4 ٱهْدِنَا ٱلصِّرَٰطَ ٱلْمُسْتَقِيمَ 5
صِرَٰطَ ٱلَّذِينَ أَنْعَمْتَ عَلَيْهِمْ 6 غَيْرِ
ٱلْمَغْضُوبِ عَلَيْهِمْ وَلَا ٱلضَّآلِّينَ 7

Suratul Fatihati

A Makka Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Bakwai

(7)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai Jinƙan talikai a duniyagabadaya, Mai jinkan Muminai A lahira a kebe.

(WANNAN SURA TA TARA KIRARI GA ALLAH MADAUKAKIN SARKI, DA BAUTAR DA MU, DA UMARNINSA DA HANINSA DA BAYANIN AL-KAWARINSA, DA NARKONSA, DA LABARAIDA ƘISSOSHI DA HIKIMOMIN AIKI; KAMAR SHIGA HANYA MA-DAIDAICIYA

1. Dukkan yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin Talikai mai rainansu.
2. Mai ni'imtawa da manya - manyan ni'imomi, mai ni'imtawa da ƙanana.
3. Sarkin Ranar.Lahira.
4. Kai kaɗai muke bautawa, kai kaɗai muke ne man taimakonka.
5. Shiryad da mu tafarki ma -daidaici.
6. Tafarkin waɗannan dakai ni'ima a garesu.
7. Ba waɗanda kayi fushi a kansu ba, (sune Yahudu). Ba ɓatattu ba. (Sune Nasara).

2 سورة البقرة مدنية 285
وآياتها مائتان وخمس وثمانون آية

بسم الله الرحمن الرحيم

الم ذلك الكتب لا ريب فيه هدى للمتقين (1)
الذين يؤمنون بالغيب ويقيمون الصلوة
ومما رزقنهم ينفقون (2) والذين يؤمنون بما أنزل
إليك وما أنزل من قبلك وبالآخرة هم يوقنون (3)
أولئك على هدى من ربهم وأولئك هم المفلحون (4)

Suratul Bakarati

A Madina Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Dari Biyu Tamanin Da Biyar (285).

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai Jinkan talikai a duniyagaba ɗaya, Mai jinkan Muminai A Lahira a keɓe.

(KIRARI GA ALKUR'AN MAIGIRMA)

1. (Allah ne masanin abinda yake nufi da wannan kalma ta) "A.L.M" Wancananka Littafi ba Kokonto a cikinsa, shiriya ne ga masu tsoron Allah.

(MASU TSORON ALLAH DA SAKAM-AKONSU)

2. Waɗanda suke bada Gaskiya da Gaibu (kamar Wutada Aljanna) suke tsaida Sallah (da haƙƙoƙinta) suke ciyarwa daga abinda muka azurta musu.
3. Da waɗannan dasuke bada gaskiya da abinda aka Saukar izuwa gareka (na daga Alƙur'ani) da abinda aka saukar daga gabanka (attaura da Injila da waninsu) Kuma sakankancewa da Ranar Lahira.
4. Waɗancananka suna kan shiriya daga Ubangijinsu, Kuma waɗancananka sune kaɗai marabauta.

(KAFIRAI DA SAKAMAKONSU)

إِنَّ الَّذِينَ كَفَرُواْ سَوَآءٌ عَلَيْهِمُۥٓ ءَآنذَرْتَهُمُۥٓ أَمْ لَمْ تُنذِرْهُمْ

لَا يُومِنُونَ (5) خَتَمَ اللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ وَعَلَىٰ سَمْعِهِمْ وَعَلَىٰ

أَبْصَٰرِهِمْ غِشَٰوَةٌ وَلَهُمْ عَذَابٌ عَظِيمٌ (6) وَمِنَ النَّاسِ

مَن يَقُولُ ءَامَنَّا بِاللَّهِ وَبِالْيَوْمِ الْآخِرِ وَمَا هُم بِمُؤْمِنِينَ (7)

يُخَٰدِعُونَ اللَّهَ وَالَّذِينَ ءَامَنُواْ وَمَا يُخَٰدِعُونَ إِلَّا

أَنفُسَهُمْ وَمَا يَشْعُرُونَ (8) فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٌ فَزَادَهُمُ

اللَّهُ مَرَضًا وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ بِمَا كَانُواْ يُكَذِّبُونَ (9) وَإِذَا قِيلَ

لَهُمْ لَا تُفْسِدُواْ فِي الْأَرْضِ قَالُوٓاْ إِنَّمَا نَحْنُ مُصْلِحُونَ (10) أَلَا إِنَّهُمْ

هُمُ الْمُفْسِدُونَ وَلَٰكِن لَّا يَشْعُرُونَ (11) وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ ءَامِنُواْ

كَمَا ءَامَنَ النَّاسُ قَالُوٓاْ أَنُومِنُ كَمَا ءَامَنَ السُّفَهَآءُ أَلَا إِنَّهُمْ

هُمُ السُّفَهَآءُ وَلَٰكِن لَّا يَعْلَمُونَ (12) ۞ وَإِذَا لَقُواْ الَّذِينَ ءَامَنُواْ ثمن

قَالُوٓاْ ءَامَنَّا وَإِذَا خَلَوْاْ إِلَىٰ شَيَٰطِينِهِمْ قَالُوٓاْ إِنَّا مَعَكُمْ إِنَّمَا نَحْنُ

مُسْتَهْزِءُونَ (13) اللَّهُ يَسْتَهْزِئُ بِهِمْ وَيَمُدُّهُمْ

فِي طُغْيَٰنِهِمْ يَعْمَهُونَ (14) أُوْلَٰٓئِكَ الَّذِينَ اشْتَرَوُاْ الضَّلَٰلَةَ

بِالْهُدَىٰ فَمَا رَبِحَت تِّجَٰرَتُهُمْ وَمَا كَانُواْ مُهْتَدِينَ (15)

5. Ƙaƙiƙa waɗanda suka kafirta daidai garesu kayi musu gargaɗi ko bakayi musu gargaɗiba, bazasu bada gaskiyaba.
6. Allah ya yimƙe a bisa zukatansu kuma akwai rufi a bisa kunnuwansu da idandinansu, da azaba madauwamiya a garesu a Ranar Lahira.

(MUNAFIKAI DA SIFOFINSU)

7. Akwai daga mutane waɗanda suke cewa mun bada gaskiya da Allah da Ranar Lahira, su ba muminai ne ba.
8. Suna Yaudarar Allah da waɗanda suka bada gaskiya, basa yaudarar kowa sai kansu, amma basuji wannan sani a jikinsu ba.
9. Akwai cuta a cikin zukatansu (shakka da nifaƙa) sai Allah ya fara masu cuta, Azaba mai raɗaɗi na garesu saboda ƙaryatawarsu (ga Ma'aikin Allah S.A.W).

(DAGA SIFOFIN MUNAFUKAI HAR YAU)

10. Idan ance dasu kada kuyi ɓarna a bayan ƙasa, sai suce mu kurum masu gyara ne.
11. To, haƙiƙa sune kaɗai maɓarnata, amma basu san (sune maɓarnata) ba.
12. Idan Ance dasu ku bada gaskiya tamfadda cikakkun mutane (Annabi da sahabbansa) suka bada gaskiya, su kAnce bazamu bada gaskiya tamfadda wawayen mutane suka bada gaskiya ba, to haƙiƙa su, sune wawaye, amma basu san haka ba.

(DAGA SIFOFIN MUNAFUKAI HAR YAU DAI)

13. Idan sun gamu da waɗanda suka bada gaskiya su kAnce mun bada gaskiya, idan sun koma izuwa shiyagabanninsu sukAnce haƙiƙa muna taredaku ,(a cikin Addini) mudai kawai masu izgili ne dasu.
14. Ubangiji yanayi musu sakamakon izgili n nan, yanayi musujinkiri a cikin shishshiginsu; suna kaikawo.
15. Waɗancananka ne waɗanda suka sai ɓata dashiriya, cinikinsu bai riba ba, basu kasance shiryayyu ba.

(SANYA MISALCE - MISALCE GA MUNAFUKAI)

مَثَلُهُمْ كَمَثَلِ الَّذِے اِسْتَوْقَدَ نَاراً فَلَمَّا أَضَآءَتْ مَا حَوْلَهُۥ ذَهَبَ اَللَّهُ
بِنُورِهِمْ وَتَرَكَهُمْ فِے ظُلُمَٰتٖ لَّا يُبْصِرُونَ (16) صُمُّۢ بُكْمٌ عُمْيٞ
فَهُمْ لَا يَرْجِعُونَ (17) أَوْ كَصَيِّبٖ مِّنَ اَلسَّمَآءِ فِيهِ ظُلُمَٰتٞ
وَرَعْدٞ وَبَرْقٞ يَجْعَلُونَ أَصَٰبِعَهُمْ فِے ءَاذَانِهِم مِّنَ اَلصَّوَٰعِقِ
حَذَرَ اَلْمَوْتِ وَاللَّهُ مُحِيطُۢ بِالْكَٰفِرِينَ (18) يَكَادُ اُلْبَرْقُ يَخْطَفُ
أَبْصَٰرَهُمْ كُلَّمَا أَضَآءَ لَهُم مَّشَوْاْ فِيهِ وَإِذَا أَظْلَمَ عَلَيْهِمْ
قَامُواْ وَلَوْ شَآءَ اَللَّهُ لَذَهَبَ بِسَمْعِهِمْ وَأَبْصَٰرِهِمْ إِنَّ اَللَّهَ
عَلَىٰ كُلِّ شَےْءٖ قَدِيرٞ (19) يَٰأَيُّهَا اَلنَّاسُ اُعْبُدُواْ رَبَّكُمُ
اُلَّذِے خَلَقَكُمْ وَالَّذِينَ مِن قَبْلِكُمْ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ (20) اَلَّذِے
جَعَلَ لَكُمُ اُلْأَرْضَ فِرَٰشاً وَالسَّمَآءَ بِنَآءً وَأَنزَلَ مِنَ اَلسَّمَآءِ
مَآءً فَأَخْرَجَ بِهِۦ مِنَ اَلثَّمَرَٰتِ رِزْقاً لَّكُمْ فَلَا تَجْعَلُواْ لِلَّهِ
أَندَاداً وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ (21) وَإِن كُنتُمْ فِے رَيْبٖ مِّمَّا نَزَّلْنَا عَلَىٰ
عَبْدِنَا فَأْتُواْ بِسُورَةٖ مِّن مِّثْلِهِۦ وَادْعُواْ شُهَدَآءَكُم مِّن دُونِ اِللَّهِ
إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ (22) فَإِن لَّمْ تَفْعَلُواْ وَلَن تَفْعَلُواْ فَاتَّقُواْ
اُلنَّارَ اَلَّتِے وَقُودُهَا اَلنَّاسُ وَالْحِجَارَةُ أُعِدَّتْ لِلْكَٰفِرِينَ (23)

16. Sufarsu (a cikin munafuncinsu) kamar mutanen da suka hura wuta (a cikin duhu) yayin data haskaka abinda yake daura dasu (suka aminee tsoro) Ubangiji ya tafi da haskensu ya barsu a cikin duffai basa ganin komai.
17. Su kurame ne (ga barin jin gaskiya) bebaye ne (ga barin fadar alheri) makafi ne (ga barin ganin gaskiya) su basa komowa (ga barin ɓata).
18. Ko, kuwa su kamar ma'abuta ruwa ne daya sakko daga hadari, akwai duffai a cikinsa da tsawa da walƙiya, suna sanya kawunan' yan yatsunsu a cikin kunnuwansu, dan kadasuji tsawawwaki, dan tsoron mutuwa. Ubangiji me kewayewa ne da kafirai (a cikin Ilmi da Iko).
19. Walƙiya tana kusata ta fyauce idondinansu, kodayaushe ta haskaka a garesu saisu tafi a cikin haskenta, idan tai duhu a garesu saisu tsaya ciki. Da Allah yaga dama da saiya tafiyar da kunnuwansu da idandunansu (na zahiri tamfar yadda ya tafiyar dana badini), haƙiƙa Ubangiji mai iko ne bisa kowane abu (daya nufa).

(TABBATADDA ALLANTAKA DA RADDI A KAN MUSHIRIKAI)

20. Yaku mutane! Ku bautawa Ubangijinku, wanda ya halicce ku (baku kasance komai ba) da waɗanda suke gabanku, ko kwa zamo masu tsoron Allah (tsoro na gaskiya)
21. Wanda yasanya ƙasa shimfiɗa a gareku, yasanya sama riƙi, ya saukad da ruwa daga hadari, ya titar daga 'ya'yan itatuwa da wannan ruwan, dan azurtawa a gareku, kadaku ,sanya ababan tarayyaga Allah, alhali ku kun san shine mahalicci.

(BAYANIN MU'UJIZAR ƘUR'ANI DA TABBATAR DA AIKIN ANNABI MUHAMMADU TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARESHI)

22. Idan kun kasance a cikin kwankwanto daga abinda muka saukar a bisa bawanmu (Annabi Muhammadu tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi na daga ƙur'ani), to, kuzo dasura daya na misalinsa, ku kirawo iyayangijinku ba Allah ba (domin su taimakeku) in kun kasance masu gaskiya (a cikin cewa Annabi Muhammadu tsira da amincin Allah su tabbata a gareshiya fade shine daga kansa).
23. Idan baku iya aikata abinda aka ambata ba, bako zaku iya aikatawa ba har abada, to, kuji tsoron wuta wacce gumagumanta kafirai da duwarwatsu, an tanajeta ga kafirai.

(WANDA YA BADA GASKIYA DA ALƘUR'ANI DA SAKAMAKONSA)

وَبَشِّرِ الذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ الصَّٰلِحَٰتِ أَنَّ لَهُمْ جَنَّٰتٖ
تَجْرِے مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَٰرُ كُلَّمَا رُزِقُواْ مِنْهَا مِن
ثَمَرَةٖ رِّزْقاٗ قَالُواْ هَٰذَا الذِے رُزِقْنَا مِن قَبْلُ وَأُتُواْ بِهِۦ
مُتَشَٰبِهاٗ وَلَهُمْ فِيهَا أَزْوَٰجٞ مُّطَهَّرَةٞ وَهُمْ فِيهَا
خَٰلِدُونَ (24) * إِنَّ اللَّهَ لَا يَسْتَحْيِۦ أَن يَضْرِبَ مَثَلاٗ مَّا (ربع)
بَعُوضَةٗ فَمَا فَوْقَهَا فَأَمَّا الذِينَ ءَامَنُواْ فَيَعْلَمُونَ
أَنَّهُ الْحَقُّ مِن رَّبِّهِمْ وَأَمَّا الذِينَ كَفَرُواْ فَيَقُولُونَ
مَاذَا أَرَادَ اللَّهُ بِهَٰذَا مَثَلاٗ يُضِلُّ بِهِۦ كَثِيراٗ وَيَهْدِے بِهِۦ
كَثِيراٗ وَمَا يُضِلُّ بِهِۦ إِلَّا الْفَٰسِقِينَ (25) الذِينَ يَنقُضُونَ
عَهْدَ اللَّهِ مِنۢ بَعْدِ مِيثَٰقِهِۦ وَيَقْطَعُونَ مَا أَمَرَ اللَّهُ
بِهِۦ أَن يُوصَلَ وَيُفْسِدُونَ فِي الْأَرْضِ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ الْخَٰسِرُونَ (26)
كَيْفَ تَكْفُرُونَ بِاللَّهِ وَكُنتُمْ أَمْوَٰتاٗ فَأَحْيَٰكُمْ
ثُمَّ يُمِيتُكُمْ ثُمَّ يُحْيِيكُمْ ثُمَّ إِلَيْهِ تُرْجَعُونَ (27) هُوَ الذِے
خَلَقَ لَكُم مَّا فِي الْأَرْضِ جَمِيعاٗ ثُمَّ اسْتَوَىٰٓ إِلَى السَّمَآءِ
فَسَوَّىٰهُنَّ سَبْعَ سَمَٰوَٰتٖ وَهُوَ بِكُلِّ شَےْءٍ عَلِيمٞ (28)

24. Yi albishir ga wadanda suka bada gaskiya da Allah sukayi ayyuka nagari da cewa Aljannatai na garesu. ƙoramu suna gudana daga ƙarƙashin itatuwanta, koyaushe aka azurta musu arziki daga gareta na daga nau'in dan itaciyatata sai suce wannan abinda aka azurta mana ne tun gaba,anzo musu dashi mai kama da juna (a launi mai saɓawa a dandano). Mataye na garesu a cikinta ababan tsarkakewa daga dukkan ƙazanta (Hurur'aini da waninsu). Su masu dauwama ne a cikinta har abada.

(MISALCE - MISALCE A CIKIN ƘUR'ANI DA MATSAYIN MUTANE A CIKINTA)

25. Ubangiji baya barin sanya misali, komai ƙanƙantarsa, sauro da abinda yafishi (saboda abinda yake cikin wannan misali na daga Hikimomi) amma waɗanda suka bada gaskiya sunsan cewa haƙiƙa shi gaskiya ne daga Ubangijinsu, amma waɗanda suka kafirta suna cewa me Allah yake nufi da wannan Misali, yana batad da yawaici (na daga kafirai) da wannan misali, yana shiryad da yawaici (na daga muminai) da wannan Misali, baya batad da kowa dashi sai makangara ga ɗa'ar Ubangiji.

26. Sune waɗanda suke warware alƙawarin Ubangiji (na bada gaskiya da Annabi Muhammadu tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi) bayan ƙarfafa shi (a kansu), suke yanke abinda Allah yayi umarni dashi a sadashi, (shine imani da Annabi da zuminci da waninsu) suke ɓarna a cikin ƙasa, (da saɓanni). Waɗancananka sune taɓaɓɓu.

(MABAYYANAN IKON ALLAH)

27. YaYakuke kafircewa da Allah? alhali haƙiƙa kun kasance. Maniyyi cikin tsatstsan iyaye, ya rayaku (a cikin Mahaifa) sannan ya karɓi ranku (yayin ƙarewar ajalin ku sannan ya rayaku (da tashin Alƙiyama) sannan izuwa a gareshi ake komar daku (bayan tashi dan sakamako).

28. Shine wanda ya halicci abinda yake cikin ƙasa baki ɗaya dan ku (dan kuyi amfani dashi kuyi izna), sannan yayi nufi azuwa sammai ya daidaita su sammai guda bakwai, Shi masanine da komai.

(KISSAR HALITTAR MUTUM DA ZA-MANSA HALIFA)

وَإِذْ قَالَ رَبُّكَ لِلْمَلَٰٓئِكَةِ إِنِّے جَاعِلٞ فِے اِ۬لْأَرْضِ خَلِيفَةٗۖ قَالُوٓاْ
أَتَجْعَلُ فِيهَا مَنْ يُّفْسِدُ فِيهَا وَيَسْفِكُ اُ۬لدِّمَآءَ وَنَحْنُ نُسَبِّحُ
بِحَمْدِكَ وَنُقَدِّسُ لَكَۖ قَالَ إِنِّيَ أَعْلَمُ مَا لَا تَعْلَمُونَۖ (29) وَعَلَّمَ
ءَادَمَ اَ۬لْأَسْمَآءَ كُلَّهَا ثُمَّ عَرَضَهُمْ عَلَى اَ۬لْمَلَٰٓئِكَةِ فَقَالَ
أَنۢبِـُٔونِے بِأَسْمَآءِ هَٰٓؤُلَآءِ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَۖ (30) قَالُواْ سُبْحَٰنَكَ
لَا عِلْمَ لَنَآ إِلَّا مَا عَلَّمْتَنَآۖ إِنَّكَ أَنتَ اَ۬لْعَلِيمُ اُ۬لْحَكِيمُۖ (31) قَالَ
يَٰٓـَٔادَمُ أَنۢبِئْهُم بِأَسْمَآئِهِمْۖ فَلَمَّآ أَنۢبَأَهُم بِأَسْمَآئِهِمْ قَالَ أَلَمْ أَقُل
لَّكُمْ إِنِّيَ أَعْلَمُ غَيْبَ اَ۬لسَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَأَعْلَمُ مَا تُبْدُونَ
وَمَا كُنتُمْ تَكْتُمُونَۖ (32) * وَإِذْ قُلْنَا لِلْمَلَٰٓئِكَةِ اِ۪سْجُدُواْ ثمن
لِأٓدَمَ فَسَجَدُوٓاْ إِلَّآ إِبْلِيسَ أَبَيٰ وَاسْتَكْبَرَ وَكَانَ مِنَ اَ۬لْكٰ۪فِرِينَۖ (33)
وَقُلْنَا يَٰٓـَٔادَمُ اُ۟سْكُنْ أَنتَ وَزَوْجُكَ اَ۬لْجَنَّةَ وَكُلَا مِنْهَا رَغَدًا حَيْثُ شِئْتُمَاۖ
وَلَا تَقْرَبَا هَٰذِهِ اِ۬لشَّجَرَةَ فَتَكُونَا مِنَ اَ۬لظَّٰلِمِينَۖ (34) فَأَزَلَّهُمَا اَ۬لشَّيْطَٰنُ
عَنْهَا فَأَخْرَجَهُمَا مِمَّا كَانَا فِيهِۖ وَقُلْنَا اَ۪هْبِطُواْ بَعْضُكُمْ لِبَعْضٍ
عَدُوّٞۖ وَلَكُمْ فِے اِ۬لْأَرْضِ مُسْتَقَرّٞ وَمَتَٰعٌ إِلَيٰ حِينٖۖ (35) فَتَلَقَّيٰٓ
ءَادَمُ مِن رَّبِّهِۦ كَلِمَٰتٖ فَتَابَ عَلَيْهِۖ إِنَّهُۥ هُوَ اَ۬لتَّوَّابُ اُ۬لرَّحِيمُۖ (36)

29. (Ka ambata ya Annabi Muham-madu) yayin da Ubangijinka yace da Mala'iku "Nizan sanya halifa a cikin kasa" (dazai zartad da hukunce - hukunce na a cikinta, shine Annabi Adamu) sukace "Ka sa kuwa a cikinta, wanda yake ɓarna a cikinta? (da sabanni) yake Zibda jinainai, alhali mu kuwa muna Tasbihi tare dayabanka, muna tsarkake ka" (ga abinda bai kamatadakai ba) Ubangiji yace "Ni na san abindabaku sani ba".

30. Yasanar da Annabi Adamu su-nayen ababan ambato dukkanta (har kwarya da masaki da Ludayi) sannan ya bijirar dasu a bisa Mala'iku sai yace dasu "Ku gaya mini sunayen waɗannan ababan ambato, in kun kasance magasgata".

31. Sukace "Tsarki ya tabbata gareka ba sani garemu sai abinda ka sanar da mu, haƙiƙa kaine masani gwani".

32. Ubangiji yace "Ya Adamu! Gayawa Mala'iku sunayan ababan ambaton", Yayin dayagaya musu sunayen, Ubangiji yace (dasu) "BAnce daku ,haƙiƙa ni na san gaibun Sammai da kassai ba? Kuma na san abindaku ,ke bayyanawa da abinda kuka kasance kuna ɓoyewa".

(GIRMAMA WAN ANNABI ADAMU DASUNKUYAR MALA'IKU A GARESHI)

33. (ka ambata) zamanin da mukace da Mala'iku kuyi sunkuyo ga An-nabi Adamu, suka sunkuya sai Iblis kaɗai ne yaki sunkuyawa yayi girman kai, ya zama daga kafirai (a cikin sanin Allah).

(MUTUM DA DABI'ARSA DA MAT-SAYIN SHAIƊAN DAGA GARESHI)

34. Muka faɗa ga Annabi Adamu, "Zauna Aljanna kai da matarka (Hauwa'u)" Kuci daga gareta ci mayalwaci; halaliya a ko'ina ku ka ga dama, kadaku, kusanci wannan itaciya da ci daga gare ta (Itace Alkama ko Inabi) kwa zama daga Azzalimai".

35. Sai Shaiɗan ya nisanta su ga bar-in Aljanna, (yace dasu "bana shiryad daku ,ba a bisa itaciyar dauwama?" Ya rantse musu da Allah haƙiƙa shi mai nasiha ne a garesu, sai suka ci daga gare ta) sai yafitad dasu daga abinda suka kasance a cikinsa (na daga ni'ima), mukace dasu "ku sauka izuwa ƙasa (kuda abinda kuka kunsa na daga zurriyarku) sha-shinku maƙiyi ne ga sashi, kuna da matabbata a ƙasa, da jin dadi izuwa ƙarewar ajalinku".

36. Sai Annabi Adamu ya karɓo kalmomi daga Ubangijinsa (Itace RABBANA ZALAMNA ANFUSANA yayi roƙo da ita) sai Allah ya ƙarbi tubansa. Haƙiƙa Ubangiji shine mai yawan karɓar tuba (ga bayinsa) maijin kai (dasu).

قُلْنَا اهْبِطُوا مِنْهَا جَمِيعًا فَإِمَّا يَأْتِيَنَّكُم مِّنِّي هُدًى فَمَن تَبِعَ
هُدَايَ فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿37﴾ وَالَّذِينَ كَفَرُوا
وَكَذَّبُوا بِآيَاتِنَا أُولَٰئِكَ أَصْحَابُ النَّارِ هُمْ فِيهَا خَالِدُونَ ﴿38﴾
يَا بَنِي إِسْرَائِيلَ اذْكُرُوا نِعْمَتِيَ الَّتِي أَنْعَمْتُ عَلَيْكُمْ وَأَوْفُوا
بِعَهْدِي أُوفِ بِعَهْدِكُمْ وَإِيَّايَ فَارْهَبُونِ ﴿39﴾ وَآمِنُوا بِمَا أَنزَلْتُ
مُصَدِّقًا لِّمَا مَعَكُمْ وَلَا تَكُونُوا أَوَّلَ كَافِرٍ بِهِ وَلَا تَشْتَرُوا بِآيَاتِي
ثَمَنًا قَلِيلًا وَإِيَّايَ فَاتَّقُونِ ﴿40﴾ وَلَا تَلْبِسُوا الْحَقَّ بِالْبَاطِلِ
وَتَكْتُمُوا الْحَقَّ وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿41﴾ وَأَقِيمُوا الصَّلَاةَ وَآتُوا الزَّكَاةَ
وَارْكَعُوا مَعَ الرَّاكِعِينَ ﴿42﴾ * أَتَأْمُرُونَ النَّاسَ بِالْبِرِّ ربع
وَتَنسَوْنَ أَنفُسَكُمْ وَأَنتُمْ تَتْلُونَ الْكِتَابَ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿43﴾
وَاسْتَعِينُوا بِالصَّبْرِ وَالصَّلَاةِ وَإِنَّهَا لَكَبِيرَةٌ إِلَّا عَلَى الْخَاشِعِينَ ﴿44﴾
الَّذِينَ يَظُنُّونَ أَنَّهُم مُّلَاقُو رَبِّهِمْ وَأَنَّهُمْ إِلَيْهِ رَاجِعُونَ ﴿45﴾
يَا بَنِي إِسْرَائِيلَ اذْكُرُوا نِعْمَتِيَ الَّتِي أَنْعَمْتُ عَلَيْكُمْ وَأَنِّي فَضَّلْتُكُمْ
عَلَى الْعَالَمِينَ ﴿46﴾ وَاتَّقُوا يَوْمًا لَّا تَجْزِي نَفْسٌ عَن نَّفْسٍ شَيْئًا
وَلَا يُقْبَلُ مِنْهَا شَفَاعَةٌ وَلَا يُؤْخَذُ مِنْهَا عَدْلٌ وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ ﴿47﴾

37. Mukace (dasu) "ku sauka daga cikinta baki daya to, idan shiriya tazo mukudaga gareni to, wadanda sukabi shiriyata suka bada gaskiya, ba tsoro a garesu (A duniya) kuma su bazasuyi ɓakin ciki ba; (a Lahira).

38. "Wadannan da suka kafirta suka ƙaryata Ayoyinmu (Litattafanmu), wadancananka sune "yan wuta, su masu dauwama ne a cikinta".

(BANI - ISRA'ILA DA ABINDA AKA NEMA DAGA GARESU)

39. Yaku Bani - Isra'ila! ku tuna ni'imata wacce nayi a gareku (watan iyayenku kamar tserarwa daga Fir'auna da sauransu) ku cika alƙawarina (shine bada gaskiya da Annabi Muhammadu tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi) na cika al ƙawarinku (shine sakamako da Aljanna) sai kuji tsorona ni kaɗai.

40. Kubada gaskiya da abinda na saukar (shine Alƙur'ani) Mai gasgatawa da abinda yake taredaku ,(shine Attaura) kadaku ,zamo farkon masu kafircewa dashi, kadaku ,musanyo tamani ƙanƙani da Ayoyina, ku kiyaye ni kaɗai.

41. Kadaku ,cuɗanyagaskiya da ƙarya, kadaku ,ɓoye gaskiya alhali kunsan gaskiyace.

42. Ku tsaida sallah (da haƙƙoƙinta na zahiri dana badini), ku bada Zakka, kuyi Sallah tareda Masallata (Annabi Sallallahu alaihi wasallama da Sahabbansa).

(MALAMAN YAHUDAWA DA HALU-LUWANSU)

43. Danme kuke umarmin mutane da aikin alheri (Imani da Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama) ku ke barin kawukanku, alhali ku kuna karanta Attaura, ashe bakwa hankaici mugun aikin kuba?

44. Ku nemi taimako da haƙuri (a cikin al'amuranku) da Salla, haƙiƙa ita (Salla) mai nauyi ce sai a gurin masu tsoron Allah.

45. Sune waɗanda suka tabbata, haƙiƙa su zasu gamu da Ubangijinsu (a Tashin ƙiyama) Kuma haƙiƙa su masu komawa ne izuwa gareshi(a ranar Lahira).

46. Yaku Bani - Isra'ila! ku tuna ni'imata wacce na ni'imta a gare ku, ku gode da Da'a, kuma hakika nina fifita iyayenku a kan mutanen zamaninsu.

47. Kuji tsoron Rana wacce wata rai bazata wadatad da wata rai komai ba a cikin wannan rana (Itace ranar Alƙiyama). Baza a karɓi fansa badaga gareta, bakuma za a hana musu azabar Allah ba.

(NU'IMOMIN ALLAH GUDA (10) BISA YAHUDAWA)

وَإِذْ نَجَّيْنَٰكُم مِّنْ ءَالِ فِرْعَوْنَ يَسُومُونَكُمْ سُوٓءَ اَ۬لْعَذَابِ يُذَبِّحُونَ
أَبْنَآءَكُمْ وَيَسْتَحْيُونَ نِسَآءَكُمْ وَفِي ذَٰلِكُم بَلَآءٌ مِّن رَّبِّكُمْ
عَظِيمٌ ﴿48﴾ وَإِذْ فَرَقْنَا بِكُمُ اُ۬لْبَحْرَ فَأَنجَيْنَٰكُمْ وَأَغْرَقْنَآ ءَالَ
فِرْعَوْنَ وَأَنتُمْ تَنظُرُونَ ﴿49﴾ وَإِذْ وَٰعَدْنَا مُوسَىٰٓ أَرْبَعِينَ لَيْلَةً
ثُمَّ اَ۪تَّخَذتُّمُ اُ۬لْعِجْلَ مِنۢ بَعْدِهِۦ وَأَنتُمْ ظَٰلِمُونَ ﴿50﴾ ثُمَّ عَفَوْنَا
عَنكُم مِّنۢ بَعْدِ ذَٰلِكَ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿51﴾ وَإِذْ ءَاتَيْنَا
مُوسَى اَ۬لْكِتَٰبَ وَالْفُرْقَانَ لَعَلَّكُمْ تَهْتَدُونَ ﴿52﴾ * وَإِذْ قَالَ
مُوسَىٰ لِقَوْمِهِۦ يَٰقَوْمِ إِنَّكُمْ ظَلَمْتُمْ أَنفُسَكُم بِاتِّخَاذِكُمُ اُ۬لْعِجْلَ
فَتُوبُوٓاْ إِلَىٰ بَارِئِكُمْ فَاقْتُلُوٓاْ أَنفُسَكُمْ ذَٰلِكُمْ خَيْرٌ لَّكُمْ
عِندَ بَارِئِكُمْ فَتَابَ عَلَيْكُمْ إِنَّهُۥ هُوَ اَ۬لتَّوَّابُ اُ۬لرَّحِيمُ ﴿53﴾
وَإِذْ قُلْتُمْ يَٰمُوسَىٰ لَن نُّؤْمِنَ لَكَ حَتَّىٰ نَرَى اَ۬للَّهَ
جَهْرَةً فَأَخَذَتْكُمُ اُ۬لصَّٰعِقَةُ وَأَنتُمْ تَنظُرُونَ ﴿54﴾ ثُمَّ بَعَثْنَٰكُم
مِّنۢ بَعْدِ مَوْتِكُمْ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿55﴾ وَظَلَّلْنَا عَلَيْكُمُ
اُ۬لْغَمَامَ وَأَنزَلْنَا عَلَيْكُمُ اُ۬لْمَنَّ وَالسَّلْوَىٰ كُلُواْ مِن طَيِّبَٰتِ
مَا رَزَقْنَٰكُمْ وَمَا ظَلَمُونَا وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمْ يَظْلِمُونَ ﴿56﴾

ثمن

48. (Ku ambata) zamanin da muka tserar da iyayenku daga Fir'auna da mutanensa suna ɗanɗana muku mummunar azaba, suna yanyanka 'ya'yanku, suna wanzad da matayanku, akwai bala'i mai girma daga Ubangijinku a cikin wancanenku (azaba).
49. (Ku ambata) zamanin da muka keta kogi sabodaku ,(kogin kulzumu) sai muka tserar daku ,(daga nitsewa muka nitsar da Fir'auna da mutanensa, alhali ku kuna duban (kifewar kogi) a kansu.
50. (Ku ambaci zamanin da muka alƙawarta wa Annabi Musa dare arba'in (zamu bashi Attaura a yayin cikarta) sannan kuka riƙi ɗan - maraki (abin bautawa) bayan tafiyarsa, (izuwa Mi'adimmu), alhali ku kuna azzalimai ga kanku dan kun ajiye bauta ba a mahallinta ba).
51. Sannan mukai rangwame ga barin ku bayan wancanenka bauta, ko kwa gode ni'mar mu a gare ku.
52. (Ku ambata) zamanin da muka baiwa Annabi Musa Attaura Itace mai rabewa tsakanin karya da gaskiya da halali da haram, ko kwa shiriya da ita daga bata.?
53. (ku ambata) zamanin da Annabi Musa ya faɗa ga mutanensa "Yaku mutanena! haƙiƙa kun zalinci kanku saboda kun mayar da ɗanmaraƙi Ubangiji, sai ku tuba izuwa ga mahaliccinku, ku kashe kawukanku, (wanda bai bautawa ɗanmaraƙi baya kashe wanda ya bauta masa) wancananku kisa shine yafi a gareku nan ga Ubangijinku, saiya karɓi tubanku, haƙiƙa shi Ubangiji mai yawan karɓar tubane mai yawan jinƙai.
54. (Ku ambata) yayin da kukace: "ya Musa! Mu bazamu bada gaskiya dan kai ba sai mun ga Allah ƙarara", tsawa ta kama ku (kuka mutu) alhali ku kuna kallon abinda ya sauka agareku (sadodasun mutune da ɗaiɗai da ɗaiɗai).
55. Sannan muka raya ku bayan kun mutu ko kwa zamo masu godewa (ni'imarmu).
56. Mukai sutura a garekuda girgije, Muka saukar agareku Darɓa da Danshila Kuci daga daɗaɗan abinda muka azurta muku (kadaku ,ɓoye, sai suka ɓoye, aka yanke musu wannan ni'inar) basu zalince muba sai dai sun kasance kansu kaɗai suke zalinta.

وَإِذْ قُلْنَا اُدْخُلُواْ هَٰذِهِ اِ۬لْقَرْيَةَ فَكُلُواْ مِنْهَا حَيْثُ شِئْتُمْ رَغَداٗ
وَادْخُلُواْ اُ۬لْبَابَ سُجَّداٗ وَقُولُواْ حِطَّةٞ يُغْفَرْ لَكُمْ خَطَٰيَٰكُمْ
وَسَنَزِيدُ اُ۬لْمُحْسِنِينَ (57) فَبَدَّلَ اَ۬لَّذِينَ ظَلَمُواْ قَوْلاً غَيْرَ اَ۬لَّذِے قِيلَ لَهُمْ
فَأَنزَلْنَا عَلَى اَ۬لَّذِينَ ظَلَمُواْ رِجْزاٗ مِّنَ اَ۬لسَّمَآءِ بِمَا كَانُواْ
يَفْسُقُونَ (58) ۞ وَإِذِ اِ۪سْتَسْقَىٰ مُوسَىٰ لِقَوْمِهِۦ فَقُلْنَا اَ۟ضْرِب ربع
بِّعَصَاكَ اَ۬لْحَجَرَ فَانفَجَرَتْ مِنْهُ اُ۪ثْنَتَا عَشْرَةَ عَيْناٗ قَدْ عَلِمَ
كُلُّ أُنَاسٖ مَّشْرَبَهُمْ كُلُواْ وَاشْرَبُواْ مِن رِّزْقِ اِ۬للَّهِ
وَلَا تَعْثَوْاْ فِے اِ۬لْأَرْضِ مُفْسِدِينَ (59) وَإِذْ قُلْتُمْ يَٰمُوسَىٰ لَن نَّصْبِرَ عَلَىٰ
طَعَامٖ وَٰحِدٖ فَادْعُ لَنَا رَبَّكَ يُخْرِجْ لَنَا مِمَّا تُنۢبِتُ اُ۬لْأَرْضُ
مِنۢ بَقْلِهَا وَقِثَّآئِهَا وَفُومِهَا وَعَدَسِهَا وَبَصَلِهَا
قَالَ أَتَسْتَبْدِلُونَ اَ۬لَّذِے هُوَ أَدْنَىٰ بِالَّذِے هُوَ خَيْرٌ
اِ۪هْبِطُواْ مِصْراٗ فَإِنَّ لَكُم مَّا سَأَلْتُمْ وَضُرِبَتْ عَلَيْهِمُ اُ۬لذِّلَّةُ
وَالْمَسْكَنَةُ وَبَآءُو بِغَضَبٖ مِّنَ اَ۬للَّهِ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ
كَانُواْ يَكْفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ اِ۬للَّهِ وَيَقْتُلُونَ اَ۬لنَّبِيٓـِٕينَ
بِغَيْرِ اِ۬لْحَقِّ ذَٰلِكَ بِمَا عَصَواْ وَّكَانُواْ يَعْتَدُونَ (60)

57. (Ku ambata) zamanin da mukace (dasu) "Ku shiga wannan alƙarya (Baitilmaƙadisi) kuci daga gareta abin yalwatawa, halaliya ta inda kuka ga dama ku shiga ƙofarta kuna masu sun-kuyo, kuce: (Abinda muke roƙo) a kankare zunubammu", a gafarta muku kurakuranku, da sannu zamu ƙarawa masu kyakkyawan aiki kyakkyawan sakamako.

58. Sai waɗanda sukayi zalinci daga garesu suka musanya magana ba wacce akace dasu ba, (suka ce: "ƙwaya a cikin gashi", suka shiga suna jan gindi) sai muka saukad da annoba a bisa waɗanda sukai zalinci, daga sama saboda fasiƙancin da suka aikata. (Mutum dubu sabai'in ya halaka daga garesu a cikin sa'a ɗaya).

59. (Ku ambata) zamanin da Annabi Musa ya nemi shayar da ruwa ga mutanensa, sai muka ce: "Doki duste da sandarka", (ya ɗoke shi) sai idaniya goma shabiyu ta keto daga gareshi, adadin 'ya'yan Yakubu) kowacce daga garesu tasan mashayarta, (mukace dasu): "Kuci kusha daga arzikin Allah, kada kuyi ɓarna a bayan ƙasa kada kuyi ɓarna".

(SASHIN MIYAGUN AYYUKAN YAHUDAWA DA ABINDA YA RISKESU)

60. (Ku ambata) zamanin da kukace "Ya Musa! Bazamu haƙura da nau'in abinci guda ɗaya ba, (Darɓa da Danshila) sai ka roƙar mana Ubangijinka yafitar mana da wani abu daga abinda ƙasa take tsirarwa, shine muɓunƙushinta, da kaluɓutunta, da alkamartada adasdinta, da albasarta". Annabi Musa yace (dasu) "Kwa dinga musanyawan abinda yake maƙaskanci da abinda yake shine mafifici?" Ku sauka wani gari, haƙiƙa abinda kuka tambaya yana gareku a cikinsa (na tsiri) aka sanya wulaƙanci da talauci a garesu, suka komo da fushi na Ubangiji. Wancananka fa saboda haƙiƙa su sun kasance suna kafircewa da ayoyin Allah ne suna kashe Annabawa (Kamar Zakariya'u da yahaya) bada gaskiya ba, wancananka -saboda sun saɓi Ubangiji ne kuma sun kasance suna shishshigi.

(DOKAR MUSULUNCI MAGAMIYA)

إِنَّ الذِينَ ءَامَنُواْ وَالذِينَ هَادُواْ وَالنَّصَٰرَىٰ وَالصَّٰبِينَ
مَنْ ءَامَنَ بِاللَّهِ وَالْيَوْمِ الْأخِرِ وَعَمِلَ صَٰلِحاً فَلَهُمُۥٓ أَجْرُهُمْ
عِندَ رَبِّهِمْ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿61﴾ وَإِذْ أَخَذْنَا
مِيثَٰقَكُمْ وَرَفَعْنَا فَوْقَكُمُ الطُّورَ خُذُواْ مَا ءَاتَيْنَٰكُم بِقُوَّةٍ
وَاذْكُرُواْ مَا فِيهِ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴿62﴾ ثُمَّ تَوَلَّيْتُم مِّنۢ بَعْدِ
ذَٰلِكَ فَلَوْلَا فَضْلُ اللَّهِ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَتُهُۥ لَكُنتُم مِّنَ الْخَٰسِرِينَ ﴿63﴾
وَلَقَدْ عَلِمْتُمُ الذِينَ اَعْتَدَواْ مِنكُمْ فِي السَّبْتِ فَقُلْنَا لَهُمْ
كُونُواْ قِرَدَةً خَٰسِـِٔينَ ﴿64﴾ فَجَعَلْنَٰهَا نَكَٰلاً لِّمَا بَيْنَ
يَدَيْهَا وَمَا خَلْفَهَا وَمَوْعِظَةً لِّلْمُتَّقِينَ ﴿65﴾ * وَإِذْ قَالَ مُوسَىٰ ثمن
لِقَوْمِهِۦٓ إِنَّ اللَّهَ يَأْمُرُكُمُۥٓ أَن تَذْبَحُواْ بَقَرَةً قَالُوٓاْ أَتَتَّخِذُنَا هُزُؤاً
قَالَ أَعُوذُ بِاللَّهِ أَنْ أَكُونَ مِنَ الْجَٰهِلِينَ ﴿66﴾ قَالُواْ
ادْعُ لَنَا رَبَّكَ يُبَيِّن لَّنَا مَا هِيَ قَالَ إِنَّهُۥ يَقُولُ إِنَّهَا بَقَرَةٌ لَّا فَارِضٌ
وَلَا بِكْرٌ عَوَانٌۢ بَيْنَ ذَٰلِكَ فَافْعَلُواْ مَا تُؤْمَرُونَ ﴿67﴾
قَالُواْ ادْعُ لَنَا رَبَّكَ يُبَيِّن لَّنَا مَا لَوْنُهَا قَالَ إِنَّهُۥ يَقُولُ
إِنَّهَا بَقَرَةٌ صَفْرَآءُ فَاقِعٌ لَّوْنُهَا تَسُرُّ النَّٰظِرِينَ ﴿68﴾

61. Wadanda suka bada gaskiya da Ubangiji da wadanda suka Yahudanta, da Nasara da duk wadanda suKafita daga addininsu, wanda ya bada gaskiya da Allah da Ranar Lahira (a zamanin Annabinmu) yayi aiki na gari (yayi aiki da shari'ar Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama), to, wadannan ladansu na garesu nan ga Ubangijinsu, ba tsoro agaresu (a duniya) baza suyi baƙin ciki ba(a Lahira).

(WANI ABU DAGA JINAYOYIN YAHUDAWA)

62. (ku ambata) zamanin da muka karɓi alƙawarinku (shine aiki da abinda yake cikin Attaura) alhali mun babbako dutse birbishinku, mukace: "Ku riƙi abinda muka bakuda ƙarfi, ku ambaci abinda yake cikinsa (Kuyi aiki dashi), ko kwa tsoraci Allah".

63. Sannan kuka bada baya bayan wancananka alƙawari, badan falalal Allah da rahamarsa a gareku ba (Tubadajinkirin azaba) da kun kasance daga cikin taɓaɓɓu.

64. Wallahi haƙiƙa kun san wadanda sukayi shishshigi daga cikinku a cikin sun kifi a ranar Asabar, (alhali an hanesu ga barinsa sune mutanen Ailata) Mukace dasu "Ku zamo birrai wulaƙantattu". (Suka zamo ita, suka halaka bayan kwana uku).

65. Muka sanya wannan uƙuba ban kashi dan izina ga al'ummar da take gabanta (watau take cikin zamaninta) da wacce za tazo bayanta, da kuma gargadi ga masu jin tsoron Allah.

(ƘISSAR YANKAN SANIYA WACCE TA ƘUNSHI FALALAR BIN I YAYE DA SHU'UMIN SABON ALLAH)

66. (Ku ambata) zamanin da Annabi Musa yake fada ga mutanensa (alhali an kashe musu wani alhali an kashe musu wani mutum ba a san wanda ya kashe shi ba) "Ubangiji yana umarnin ku ku yanka saniya (kowace iri)" suka ce: "Ka riƙe mu abin izgili ne?" Yace, "Ina neman tsari da Allah daga in zama daga masu izgili "

67. Suka ce: "Roƙar mana Ubangijinka ya bayyana mana meye ita (shekararta?"Annabi Musa) yace, "Haƙika Ubangiji yana cewa ita saniyace ba tsohuwa ba, ba yarinya ba, safe (watau tsakatsaka) tsakanin wancananka (shekaru); to, ku aikata abinda ake umarnin ku dashi (na yanka ta)".

68. Sukace "Roƙar mana Ubangijin-ka ya bayyana mana me ye launinta," Yace: "Ubangiji yana cewa ita saniyace yar ana mai gunyal launinta, tana faranta wa masu kallonta rai".

قَالُواْ اُ۟دْعُ لَنَا رَبَّكَ يُبَيِّن لَّنَا مَا هِيَ إِنَّ اَ۬لْبَقَرَ تَشَٰبَهَ عَلَيْنَا
وَإِنَّا إِن شَآءَ اَ۬للَّهُ لَمُهْتَدُونَ ﴿69﴾ قَالَ إِنَّهُۥ يَقُولُ إِنَّهَا بَقَرَةٞ
لَّا ذَلُولٞ تُثِيرُ اُ۬لْأَرْضَ وَلَا تَسْقِي اِ۬لْحَرْثَ مُسَلَّمَةٞ لَّا شِيَةَ فِيهَا
قَالُواْ ءَآلْـَٰٔنَ جِئْتَ بِالْحَقِّ فَذَبَحُوهَا وَمَا كَادُواْ يَفْعَلُونَ ﴿70﴾ وَإِذْ قَتَلْتُمْ
نَفْساً فَادَّٰرَٰٔتُمْ فِيهَا وَاللَّهُ مُخْرِجٞ مَّا كُنتُمْ تَكْتُمُونَ ﴿71﴾ فَقُلْنَا اَ۟ضْرِبُوهُ
بِبَعْضِهَا كَذَٰلِكَ يُحْيِ اِ۬للَّهُ اُ۬لْمَوْتَىٰ وَيُرِيكُمْ ءَايَٰتِهِۦ لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿72﴾
ثُمَّ قَسَتْ قُلُوبُكُم مِّنۢ بَعْدِ ذَٰلِكَ فَهْيَ كَالْحِجَارَةِ أَوْ أَشَدُّ قَسْوَةٗ
وَإِنَّ مِنَ اَ۬لْحِجَارَةِ لَمَا يَتَفَجَّرُ مِنْهُ اُ۬لْأَنْهَٰرُ وَإِنَّ مِنْهَا لَمَا يَشَّقَّقُ
فَيَخْرُجُ مِنْهُ اُ۬لْمَآءُ وَإِنَّ مِنْهَا لَمَا يَهْبِطُ مِنْ خَشْيَةِ اِ۬للَّهِ
وَمَا اَ۬للَّهُ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعْمَلُونَ ﴿73﴾ أَفَتَطْمَعُونَ أَن يُؤْمِنُواْ
لَكُمْ وَقَدْ كَانَ فَرِيقٞ مِّنْهُمْ يَسْمَعُونَ كَلَٰمَ اَ۬للَّهِ
ثُمَّ يُحَرِّفُونَهُۥ مِنۢ بَعْدِ مَا عَقَلُوهُ وَهُمْ يَعْلَمُونَ ﴿74﴾
* وَإِذَا لَقُواْ اُ۬لَّذِينَ ءَامَنُواْ قَالُواْ ءَامَنَّا وَإِذَا خَلَا حزب
بَعْضُهُمْ إِلَىٰ بَعْضٖ قَالُواْ أَتُحَدِّثُونَهُم بِمَا فَتَحَ اَ۬للَّهُ
عَلَيْكُمْ لِيُحَآجُّوكُم بِهِۦ عِندَ رَبِّكُمْ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿75﴾

69. Sukace "Roƙar mana Ubangijin-ka, ya bayyana mana Menene ita (a rayuwarta, sa'sakai take ko tana yiwa mai ita aiki) haƙiƙa jinsin saniyar ya rikita garemu, haƙiƙa mu masu shiriya ne in Allah ya yarda". (A cikin hadisi da basuyi togo bada ba a bayyana musu ba har abada).

70. Yace, "Shi yana cewa ita saniyace ba horarriyace da aiki take motsa ƙasaba, bakuma ta shayar da shuka, sumul take, babu launi a cikinta wanin Launinta", sukace "A yanzu kazo. da mabayyaniyar gaskiya", (suka same ta gurin wani ɗan saurayi mai bin uwarsa, suka sayetada cikin salkarta na dinare) suka yanka ta kamar basa aikata ba. (saboda tsadar kudinta, a cikin Hadisi dasun yanka kowace saniya da ta'isar musu, sai dai sun tsananta wa kansune sai Allah ya tsananta musu).

71. Dayayin da kuka kashe kai, sai ku kai jefefeniya a cikinta, Allah mai bayyana abinda kuka kasance kuna boyewa ne (na al'amarinta).

72. Sai mukace "Doki mataccen nan da sashinta" (suka doke shi da harshenta, saiya tashi yace: wane da wanene suka kashe ni 'ya'yan Baffansa, ya mutu aka hana su gadonsa aka kashe su) kamar wancananka (rayawa) Allah yake raya matattu, Yake nuna muku ayoyinsa don kuyi amfani da hankalinku.

(ƘASĀWAR ZUCIYAR YAHUDAWA TA GARGAJIYA)

73. Sannan zukatanku (ku Yahudawa) ta ƙeƙashe bayan wacanaiika (abin ambato raya inatacce da sauransu) ita kamar dutse ce ko mafi tsauri daga dustse a ƙeƙasa, haƙiƙa akwai daga duwatsu wanda ƙoramu suke kwararowa daga gareshi, akwai daga gare ta wanda yake kecewa sai ruwa yafito daga gareshi, akwai daga gareta wanda yake kwaranyowa daga sama, don tsoron Allah, Allah ba marabkani bane ga barin abindaku ,ke aikatawa ba.

(NISANTAWAR IMANIN YAHUDU A ZAMANIN MANZON ALLAH SAL-LALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

74. (Yaku muminai!) kada kuyi tsammanin imanin Yahudawa danku, haƙiƙa mutane sun kasance daga garesu suna jin zancan Allah (a cikin Attaura) san-nan sujirkita shi bayan sun fahince shi, alhali su sunsan (maƙaryata ne su).

75.Idan (munafukan Yahudawa) suka gamu da waɗanda suka bada gaskiya, su kance "mun gasgata cewa (Annabi Muhammadu S.A.W. shine Annabinda akayi albishir dashi a Littafinmu), Idan sashinsu yakoma zuwa shashi, sai shuwa gabanninsu (waɗanda basuyi munafinci basuce da waɗanda sukai munafunci), "Danme kuke gaya musu abinda Allah yayi budi dashi agareku (a cikin Attaura, shine kamannin Annabi Muhammadu S.A.W.) dan su kashe ku dashi nan ga Ubangijin ku (a Lahira), ashe bakwayi amfani da hankalinku ba?".

أَوَلَا يَعْلَمُونَ أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا يُسِرُّونَ وَمَا يُعْلِنُونَ ﴿76﴾ وَمِنْهُمْ
أُمِّيُّونَ لَا يَعْلَمُونَ ٱلْكِتَٰبَ إِلَّآ أَمَانِيَّ وَإِنْ هُمْ إِلَّا يَظُنُّونَ ﴿77﴾
فَوَيْلٌ لِّلَّذِينَ يَكْتُبُونَ ٱلْكِتَٰبَ بِأَيْدِيهِمْ ثُمَّ يَقُولُونَ
هَٰذَا مِنْ عِندِ ٱللَّهِ لِيَشْتَرُوا۟ بِهِۦ ثَمَنًا قَلِيلًا فَوَيْلٌ لَّهُم
مِّمَّا كَتَبَتْ أَيْدِيهِمْ وَوَيْلٌ لَّهُم مِّمَّا يَكْسِبُونَ ﴿78﴾
وَقَالُوا۟ لَن تَمَسَّنَا ٱلنَّارُ إِلَّآ أَيَّامًا مَّعْدُودَةً قُلْ
أَتَّخَذتُّمْ عِندَ ٱللَّهِ عَهْدًا فَلَن يُخْلِفَ ٱللَّهُ عَهْدَهُۥٓ
أَمْ تَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿79﴾ بَلَىٰ مَن كَسَبَ
سَيِّئَةً وَأَحَٰطَتْ بِهِۦ خَطِيٓـَٔاتُهُۥ فَأُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ
هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿80﴾ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَنَّةِ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿81﴾ وَإِذْ أَخَذْنَا
مِيثَٰقَ بَنِيٓ إِسْرَٰٓءِيلَ لَا تَعْبُدُونَ إِلَّا ٱللَّهَ وَبِٱلْوَٰلِدَيْنِ
إِحْسَانًا وَذِي ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَٰمَىٰ وَٱلْمَسَٰكِينِ
وَقُولُوا۟ لِلنَّاسِ حُسْنًا وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ
ثُمَّ تَوَلَّيْتُمْ إِلَّا قَلِيلًا مِّنكُمْ وَأَنتُم مُّعْرِضُونَ ﴿82﴾

76. (Allah yace: "Suna fadan haka) shin basu san Allah yasan abinda suke ɓoyewa bane da abinda suke bayyanawa?".
77. Akwai daga garesu jahilai basu san Attaura ba sai ƙaryace ƙaryace (da suka karɓa daga shuwagabanninsu) su basu kasance (a cikin musun Annabi Muhammadu) ba, sai masuyin zato kawai.

(ƘARYAR MALAMAN YAHUDAWA DA ƘIRƘIRENSU A BISA UBANGIJI)

78. Tsananin azabaya tabbata ga waɗanda suke rubuta Littafi da hannayensu (abin ƙirƙira), domin su misanyo kudi ƙanƙani dashi (na duniya, sune Yahudu, sun gyara sifar Annabi da ayar rajimi sun rubutata a sabanin yadda aka saukar).Tsananin azabana garesu saboda abinda hannayensu ta rubuta, kuma har yau tsananin azabana garesu saboda abinda suke tsomrta (na rashwawa)!.
79. Sukace (a yayin da Annabi ya basu tsoro da Wuta) "Bazata taɓamuba sai'yan kwanika kaɗan (kwana arba'in na bautar dan maraƙi". (Ya Annabi Muhammadu!) Cene (dasu) "Kun riƙi alƙawari da wannan ne a wurin Ubangiji, to, Allah bazai saɓa alƙawarinsa dashi ba?" (A'a) bari ku dai kuna ƙirƙiron abinda baku sanibane ga Allah.
80. E, zaku shiga wuta waɗanda suka aikata shirka miyagun ayyukansu suka kewaye dasu waɗancananka su ne'yan wuta, su masu dauwama ne a cikinta.
81. Waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagari, wadancananka sune'yan Aljanna, su masu dauwamane a cikinta.

(SABAWAN YAHUDAWA GA AL-ƘAWURRA)

82. (Ka ambata) zamanin da muka riƙi alƙawarin Bani - Isra'ila (a cikin Attaura) mukace, "Ba kwa bautawa kowa sai Allah (Watau kadaku ,bautawa kowa sai shi) ku kyautata ga mahaifa kyautatawa, da ma'abota zumuntada marayu da miskinai, ku faɗawa mutane magana kyakkyawa (amri da ma'arufi da hani ga munkari da gaskiya cikin sha'anin Annabi Sallallahu alaihi wasallama) ku tsaida salla tareda haƙƙoƙinta (na zahiri dana baɗini) ku bada Zakka", (kuka karɓi wancananka) sannan kuka bada bayaga barin cikawa dashi (wato iyayensu) sai kadan daga gareku, alhali kuna masu bijirewa ga barinsa.

(WANI ABU DAGA SABAWAN YAHUDAWA GA ALƘAWARI)

وَإِذْ أَخَذْنَا مِيثَٰقَكُمْ لَا تَسْفِكُونَ دِمَآءَكُمْ وَلَا تُخْرِجُونَ
أَنفُسَكُم مِّن دِيَٰرِكُمْ ثُمَّ أَقْرَرْتُمْ وَأَنتُمْ تَشْهَدُونَ ﴿83﴾
ثُمَّ أَنتُمْ هَٰٓؤُلَآءِ تَقْتُلُونَ أَنفُسَكُمْ وَتُخْرِجُونَ
فَرِيقًا مِّنكُم مِّن دِيَٰرِهِمْ تَظَّٰهَرُونَ عَلَيْهِم بِالْإِثْمِ
وَالْعُدْوَٰنِ * وَإِن يَأْتُوكُمْ أُسَٰرَىٰ تُفَٰدُوهُمْ وَهُوَ
مُحَرَّمٌ عَلَيْكُمْ إِخْرَاجُهُمْ أَفَتُؤْمِنُونَ بِبَعْضِ الْكِتَٰبِ
وَتَكْفُرُونَ بِبَعْضٍ فَمَا جَزَآءُ مَن يَفْعَلُ ذَٰلِكَ مِنكُمْ
إِلَّا خِزْيٌ فِي الْحَيَوٰةِ الدُّنْيَا وَيَوْمَ الْقِيَٰمَةِ يُرَدُّونَ إِلَىٰ أَشَدِّ
الْعَذَابِ وَمَا اللَّهُ بِغَٰفِلٍ عَمَّا يَعْمَلُونَ ﴿84﴾ أُولَٰٓئِكَ الَّذِينَ
اشْتَرَوُا الْحَيَوٰةَ الدُّنْيَا بِالْآخِرَةِ فَلَا يُخَفَّفُ عَنْهُمُ الْعَذَابُ
وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ ﴿85﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَى الْكِتَٰبَ وَقَفَّيْنَا مِنۢ بَعْدِهِۦ
بِالرُّسُلِ وَءَاتَيْنَا عِيسَى ابْنَ مَرْيَمَ الْبَيِّنَٰتِ وَأَيَّدْنَٰهُ بِرُوحِ
الْقُدُسِ أَفَكُلَّمَا جَآءَكُمْ رَسُولٌ بِمَا لَا تَهْوَىٰ أَنفُسُكُمُ اسْتَكْبَرْتُمْ
فَفَرِيقًا كَذَّبْتُمْ وَفَرِيقًا تَقْتُلُونَ ﴿86﴾ وَقَالُوا قُلُوبُنَا غُلْفٌ
بَل لَّعَنَهُمُ اللَّهُ بِكُفْرِهِمْ فَقَلِيلًا مَّا يُؤْمِنُونَ ﴿87﴾

ثمن

83. Da lokacin da muka riƙi alƙawarinku, muka ce: "Ba kwa zibda jinainanku (watau kadaku ,zubar da ita) ba kwa fitad da kaw-ukanku daga gidaddajinsu (watau kada sashenku yafitad da sashenku daga gidansa) "Sannan kuka yarda da wannan alƙawari, alhali ku kuna shaidad da wannan a bisa kawunanku.

84. Sannan ku Yaku Waɗannan kuna kashe kawukanku, kuna fitad da waɗansu mutane daga cikinku daga gidaddajinsu, kuna taimako a kansu da sabo da zalinci, in sun zo muku suna ribatattu kuna fansassu, alhali shi wannan al'amari an haramta fisshesu a gareku, danme kuke bada gaskiya da sashen littafi (watau fansa) kuke kafircewa da sashe (barin kisa da barin fitarwa, da barin tarandangi?) Ba sakamakon wanda yake aikata wancananka sai kunyata a rayuwar duniya (sun kunyatada kashe kuraizatu da kore Nalim izuwa Sham da dora jiziya a kansu) ranar alƙiyama za a mai dasu izuwa mafi tsananin azaba, Allah ba marabkanibane ga abinda suke aikatawa ba

85. Wadancananka sune waɗanda suka sayi rayuwar duniya maimakon Lahira, baza a sauwaƙe azabar Allah ga barin su ba, su baza a hana musu azabar Allah ba.

(MATSAYIN YAHUDAWA DAGA MANZANNI DA LITTATTAFAI ABA-BAN SAUKARWA) WANDA YA ƘUNSHI HALACCIN TAWASSULI (WATO ISANAN TUWA) DA MA AIKIN ALLAH ('S.A.W)

86. Haƙiƙa mun baiwa Annabi Musa Attaura mun biyar da Manzanni daga bayansa, mun baiwa Annabi Isa dan Maryama Mu'ujuzozi (kamar raya matattu da sauransu) Mun karfafa shi da ran tsarki (Mala'ika jibrilu yana tafiya tare dashi inda duk ya tafi kuka ƙi daidaituwa) Yanzu kwa ringa yin girman kai a kowane lokaci manzo yazo mukuda abinda kawunanku bata so? Sai ku karyata waɗansu daga cikinsu, waɗansu koku kashe su. (Kamar Annabi Zakariya'u da - Yahaya!).

87. Sukace (da Annabi don izgili) "zukatanmu rufaffu ne bata kiyaye abinda kake fada", to, Ubangiji yace: "Bari Allah ya tsine musu albarka ne saboda kafircinsu, to kaɗan ne ƙwarai suke bada gaskiya".

وَلَمَّا جَآءَهُمْ كِتَٰبٌ مِّنْ عِندِ ٱللَّهِ مُصَدِّقٌ لِّمَا مَعَهُمْ وَكَانُواْ
مِن قَبْلُ يَسْتَفْتِحُونَ عَلَى ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فَلَمَّا جَآءَهُم
مَّا عَرَفُواْ كَفَرُواْ بِهِۦ فَلَعْنَةُ ٱللَّهِ عَلَى ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿88﴾ بِئْسَمَا
ٱشْتَرَوْاْ بِهِۦٓ أَنفُسَهُمْ أَن يَكْفُرُواْ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ بَغْيًا
أَن يُنَزِّلَ ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ
فَبَآءُو بِغَضَبٍ عَلَىٰ غَضَبٍ وَلِلْكَٰفِرِينَ عَذَابٌ مُّهِينٌ ﴿89﴾
وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ ءَامِنُواْ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ قَالُواْ نُؤْمِنُ بِمَآ
أُنزِلَ عَلَيْنَا وَيَكْفُرُونَ بِمَا وَرَآءَهُۥ وَهُوَ ٱلْحَقُّ مُصَدِّقًا لِّمَا مَعَهُمْ
قُلْ فَلِمَ تَقْتُلُونَ أَنۢبِيَآءَ ٱللَّهِ مِن قَبْلُ إِن كُنتُم
مُّؤْمِنِينَ ﴿90﴾ * وَلَقَدْ جَآءَكُم مُّوسَىٰ بِٱلْبَيِّنَٰتِ
ثُمَّ ٱتَّخَذْتُمُ ٱلْعِجْلَ مِنۢ بَعْدِهِۦ وَأَنتُمْ ظَٰلِمُونَ ﴿91﴾
وَإِذْ أَخَذْنَا مِيثَٰقَكُمْ وَرَفَعْنَا فَوْقَكُمُ ٱلطُّورَ
خُذُواْ مَآ ءَاتَيْنَٰكُم بِقُوَّةٍ وَٱسْمَعُواْ قَالُواْ سَمِعْنَا وَعَصَيْنَا
وَأُشْرِبُواْ فِى قُلُوبِهِمُ ٱلْعِجْلَ بِكُفْرِهِمْ قُلْ بِئْسَمَا
يَأْمُرُكُم بِهِۦٓ إِيمَٰنُكُمْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿92﴾

ربع

88. Yayin da Littafi yazo musu daga wurin Ubangiji (Alƙur'ani) mai gasgatawar abinda yake taredasu (Attaura) suka kafirce dashi. sun kasance gaban zuwansa suna neman taimako dashi a kan wadanda suka kafirta, (suna cewa Ubangiji taimakemu a kansu dan Annabindaza a aiko a ƙarshen zamani) yayin da abinda suka sani na gaskiya yazo musu (shine aiko Annabi Muhammadu) suka kafirce dashi (dan hassada da tsoro kan shugabanci) to, tsinewar Allah ta tabbata a bisa kafirai.

89. Abinda suka saida kawukansu dashiya mugusta (shine kafirtarsu da abinda Allah ya saukar na alƙur'ani) dan hassada a kan Allah ya saukar daga falalarsa (Wahayi) a bisa wanda yaso daga bayinsa sai suka komo da fushin Allah saboda kafirtarsu da Alƙur'ani) bisa fushin Allah (na tozarta Attaura da kafirtada Annabi Isa). Azaba mai wulaƙantarwa ta tabbata ga kafirai.

90. Idan ance dasu "ku bada gaskiya da abinda Allah ya saukar (alƙur'ani da waninsa)" sai suce: "Mu mun bada gaskiya da abinda aka saukar a garemu (Attaura: Ubangiji yace) "Alhali suna kafircewa da abinda ya wanince shi, shine ko gaskiya mai gasgatawan abinda yake taredasu," cene (dasu): "To, danme kuka kashe Annabawan Allah tun gaba in kun kasance masu bada gaskiya (da Attaura?").

(ƘARYAR YAHUDAWA A CIKIN DA'AWARSU TA IMANI DA ATTAURA)

91. Haƙiƙa Annabi Musa yazo mukuda mu'ujizozi (kamar sanda da hannu) sannan kuka maida dan maraki ubangiji bayan tafiyarsa izuwa Mikati alhali kuna azzalimai da bautarsa.

92. (Ka ambata) zamanin da muka riƙi alƙawarin ku (kan aiki da abinda yake cikin Attaura) alhali mun babbako dutse birbishinku, mukace: "Ku riƙi abinda muka bakuda ƙarfi kuji (umarninsa jin karɓa,)" sukace: "Munji (maganarka,) bamu karɓa ba", An cuɗanya musu son ɗanmaraƙi a cikin zukatansu saboda kafircinsu, cene (dasu) "Tir da abinda imaninku yake umarninku dashi (bautar ɗanmaraƙi) in kun kasance muminai (ai ba muminai ne ku ba!)".

(YAHUDU DA KWADAYINSU A KAN RAYUWAR DUNIYA)

قُلْ إِن كَانَتْ لَكُمُ الدَّارُ الْآخِرَةُ عِندَ اللَّهِ خَالِصَةً
مِّن دُونِ النَّاسِ فَتَمَنَّوُا الْمَوْتَ إِن كُنتُمْ صَادِقِينَ ﴿93﴾
وَلَن يَتَمَنَّوْهُ أَبَدًا بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ وَاللَّهُ عَلِيمٌ
بِالظَّالِمِينَ ﴿94﴾ وَلَتَجِدَنَّهُمْ أَحْرَصَ النَّاسِ عَلَىٰ حَيَاةٍ
وَمِنَ الَّذِينَ أَشْرَكُوا يَوَدُّ أَحَدُهُمْ لَوْ يُعَمَّرُ أَلْفَ سَنَةٍ
وَمَا هُوَ بِمُزَحْزِحِهِ مِنَ الْعَذَابِ أَن يُعَمَّرَ وَاللَّهُ بَصِيرٌ
بِمَا يَعْمَلُونَ ﴿95﴾ قُلْ مَن كَانَ عَدُوًّا لِّجِبْرِيلَ فَإِنَّهُ نَزَّلَهُ
عَلَىٰ قَلْبِكَ بِإِذْنِ اللَّهِ مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ وَهُدًى
وَبُشْرَىٰ لِلْمُؤْمِنِينَ ﴿96﴾ مَن كَانَ عَدُوًّا لِّلَّهِ وَمَلَائِكَتِهِ
وَرُسُلِهِ وَجِبْرِيلَ وَمِيكَائِيلَ فَإِنَّ اللَّهَ عَدُوٌّ لِّلْكَافِرِينَ ﴿97﴾
وَلَقَدْ أَنزَلْنَا إِلَيْكَ آيَاتٍ بَيِّنَاتٍ وَمَا يَكْفُرُ بِهَا
إِلَّا الْفَاسِقُونَ ﴿98﴾ أَوَكُلَّمَا عَاهَدُوا عَهْدًا نَّبَذَهُ فَرِيقٌ مِّنْهُم
بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿99﴾ وَلَمَّا جَاءَهُمْ رَسُولٌ مِّنْ عِندِ اللَّهِ
مُصَدِّقٌ لِّمَا مَعَهُمْ نَبَذَ فَرِيقٌ مِّنَ الَّذِينَ أُوتُوا الْكِتَابَ
كِتَابَ اللَّهِ وَرَاءَ ظُهُورِهِمْ كَأَنَّهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿100﴾

93. Cene (dasu:) " Idan gidan Lahira (Aljanna) ta kasance keɓantacciya daukuna na Allah, batareda kowaba (tamfad dakuda riya) to, ku guraci mutuwa in kun kasance magasgata".

94. Bakuma zasu guraceta ba har abada saboda abinda hannuwansu ta gabatar (na kafircewa dashi (Sallallahu alaihi wasallama), Allah masanine da kafirai.

95. Wallahi zaka samesu mafi kwaɗayin mutane a bisa rayuwa, kuma mafi kwaɗayi daga mushirikai, ɗayansu yana gurin ya rayu shekara dubu, raya shi kuwa bashine mai nisanta shi daga azabar Ubangiji ba, Allah masanin abinda suke aikatawa

(MATSAYIN YAHUDAWA DAGA MALA'IKU TSARKAKU)

96. Cene (dasu): "Wanda ya kasance magabaci ga Jibrilu (ya mutu dan fushi) to, shine ya saukar da Alƙur'ani a bisa zuciyarka da izinin Ubangiji, mai gasgatawa da abinda yake gabansa (na daga Littattafai) kuma shiriya ne (daga bata), da al'bishir da Aljanna ga muminai.

97. Duk wanda ya kasance magabaci ga Allah da Mala'ikunsa, da manzanninsa, da Jibrila da Mika'ila, to, Ubangiji magabaci ne ga kafirai.

(WANI ABU DAGA MIYAGUN AYYUKANSU HAR YAU)

98. Haƙiƙa mun saukar da ayoyi mabayyana a gareka (Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama, raddi ne ga Dan suriya dayace dashi "Bakazo manada komai ba") ba mai kafircewa da ita sai fasiƙai.

99. Yanzu (sa kafirce da ita?) kuma koyaushe sukayi alƙawari (da Allah) alƙawari (a bisa bada gaskiya da Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama, sai wasu jama'a daga cikinsu su warware? Kai! yawaicinsu basu bada gaskiya ba.

100. Yayin da manzo daga Allah yazo musu (shine Sallallahu alai-hi wasallama), mai gasgatawa ga abinda yake taredasu, wasu jama'a daga waɗanda aka basu littafi sai suka jefar da littafin Allah a bayan bayansu, kai kace su basu san abinda yake cikinta ba.

(WANI ABU DAGA MIYAGUN AYYU-KANSU HAR YAU)

ثمن

* وَاتَّبَعُواْ مَا تَتْلُواْ الشَّيَٰطِينُ عَلَىٰ مُلْكِ سُلَيْمَٰنَ وَمَا كَفَرَ
سُلَيْمَٰنُ وَلَٰكِنِ الشَّيَٰطِينُ كَفَرُواْ يُعَلِّمُونَ النَّاسَ السِّحْرَ
وَمَا أُنزِلَ عَلَى الْمَلَكَيْنِ بِبَابِلَ هَٰرُوتَ وَمَٰرُوتَ وَمَا يُعَلِّمَٰنِ
مِنْ أَحَدٍ حَتَّىٰ يَقُولَا إِنَّمَا نَحْنُ فِتْنَةٌ فَلَا تَكْفُرْ
فَيَتَعَلَّمُونَ مِنْهُمَا مَا يُفَرِّقُونَ بِهِۦ بَيْنَ الْمَرْءِ وَزَوْجِهِۦ
وَمَا هُم بِضَآرِّينَ بِهِۦ مِنْ أَحَدٍ إِلَّا بِإِذْنِ اللَّهِ وَيَتَعَلَّمُونَ
مَا يَضُرُّهُمْ وَلَا يَنفَعُهُمْ وَلَقَدْ عَلِمُواْ لَمَنِ اشْتَرَىٰهُ
مَا لَهُۥ فِي الْآخِرَةِ مِنْ خَلَٰقٍ وَلَبِئْسَ مَا شَرَوْاْ بِهِۦ
أَنفُسَهُمْ لَوْ كَانُواْ يَعْلَمُونَ ﴿101﴾ وَلَوْ أَنَّهُمْ ءَامَنُواْ وَاتَّقَوْاْ
لَمَثُوبَةٌ مِّنْ عِندِ اللَّهِ خَيْرٌ لَّوْ كَانُواْ يَعْلَمُونَ ﴿102﴾
يَٰأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَقُولُواْ رَٰعِنَا وَقُولُواْ انظُرْنَا
وَاسْمَعُواْ وَلِلْكَٰفِرِينَ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿103﴾ مَّا يَوَدُّ الَّذِينَ
كَفَرُواْ مِنْ أَهْلِ الْكِتَٰبِ وَلَا الْمُشْرِكِينَ أَن يُنَزَّلَ
عَلَيْكُم مِّنْ خَيْرٍ مِّن رَّبِّكُمْ وَاللَّهُ يَخْتَصُّ
بِرَحْمَتِهِۦ مَن يَشَآءُ وَاللَّهُ ذُو الْفَضْلِ الْعَظِيمِ ﴿104﴾

101. Sukabi abinda shaiɗanu suka karanta a bisa zamanin mulkin Annabi Sulaimanu, Annabi Sulaimanu bai kafirta ba (ai bai aikata sihiri ba) sai dai shaiɗanu ne suka kafirta, suna sanad da mutane sihiri, da abinda aka saukar a bisa Mala'iku guda biyu a Babila, Haruta, da Maruta, basa sanad da wani face sunce "mudai fitina ne kawai, to, kadaka kafirta," saisu nemi sani a garesu na abinda zasu rarrabe tsakanin mutum da matarsa,su ba masu cutar kowa bane da sihirin saida izinin Allah, suna neman sanin abindazai cuce su bazai amfane su ba, (shine tsafi) wallahi sun sani wanda ya sayo wannan tsafi bashi da rabo a Lahira, abinda suka saida kawukansu dashiya mugusta, dasun kasance sunsan (haƙiƙar ƙarshansu).

102. Wallahi (yahudawa) sun sani dasun bada gaskiya sunji tsoron Allah (da an yi musu kyakkyawan sakamako) Wallahi sakamako na daga Ubangiji, yafi (abinda suka saida kawukansu dashi) dasun kasance sunsanshi yafi alhairi (a garesu da basu fifita wani abu a kansa ba).

(LADABI DA FISKANTARWA)

103. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! kada kuce (da Annabi Sallallahu alaihi wasallama) "Kiyaye mu" kuce "bubo izuwa garemu", kuji (abinda ake umarninku dashi jin karɓa) azaba mai raɗaɗi ta tabbata ga kafirai.

104. Waɗanda suka kafirta daga Ahlil - kitabi da Mushirikai basa gurin a saukad da wani abu na alhairi daga Ubangijinku, Allah yana keɓantar wanda yaga dama da Annabcinsa, Ubangiji ma'abocin falala ne mai girma.

(AYOYIN SHAFE HUKUNCI)

رُبع

* مَا نَنسَخْ مِنْ ءَايَةٍ أَوْ نُنسِهَا نَأْتِ بِخَيْرٍ مِّنْهَا أَوْ مِثْلِهَا
أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ اللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ﴿105﴾ أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ اللَّهَ
لَهُۥ مُلْكُ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ اللَّهِ
مِن وَلِيٍّ وَلَا نَصِيرٍ ﴿106﴾ أَمْ تُرِيدُونَ أَن تَسْـَٔلُوا رَسُولَكُمْ
كَمَا سُئِلَ مُوسَىٰ مِن قَبْلُ وَمَن يَتَبَدَّلِ الْكُفْرَ بِالْإِيمَٰنِ
فَقَدْ ضَلَّ سَوَآءَ السَّبِيلِ ﴿107﴾ وَدَّ كَثِيرٌ مِّنْ أَهْلِ الْكِتَٰبِ لَوْ يَرُدُّونَكُم
مِّنۢ بَعْدِ إِيمَٰنِكُمْ كُفَّارًا حَسَدًا مِّنْ عِندِ أَنفُسِهِم مِّنۢ بَعْدِ
مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ الْحَقُّ فَاعْفُوا وَاصْفَحُوا حَتَّىٰ يَأْتِيَ اللَّهُ بِأَمْرِهِۦٓ
إِنَّ اللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ﴿108﴾ وَأَقِيمُوا الصَّلَوٰةَ
وَءَاتُوا الزَّكَوٰةَ وَمَا تُقَدِّمُوا لِأَنفُسِكُم مِّنْ خَيْرٍ
تَجِدُوهُ عِندَ اللَّهِ إِنَّ اللَّهَ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿109﴾
وَقَالُوا لَن يَدْخُلَ الْجَنَّةَ إِلَّا مَن كَانَ هُودًا أَوْ نَصَٰرَىٰ
تِلْكَ أَمَانِيُّهُمْ قُلْ هَاتُوا بُرْهَٰنَكُمْ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿110﴾
بَلَىٰ مَنْ أَسْلَمَ وَجْهَهُۥ لِلَّهِ وَهُوَ مُحْسِنٌ فَلَهُۥٓ أَجْرُهُۥ
عِندَ رَبِّهِۦ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿111﴾

105. In muka shafe wata aya, ko muka mantad da ita, mazoda mafi amfani daga gareta (a cikin sauƙi da yawan lada) ko kamarta (a cikin taklifi da Lada) ai kasani Ubangiji mai iko ne shi bisa komai.
106. Ai kasani haƙiƙa mulkin sammai da ƙassaina Allah ne (yana aikata abinda yaga dama a cikin su), bakuda wani majibinci dazai kiyayeku ba Allah ba, wala mai hana muku azaba.
107. Bari! Shin kuna nufin ku tambayi manzankune tamfad da aka tambayi Annabi Musa tun gaba, (Shine fadinsu nuna mana Allah a sarari?) Duk wanda ya musanya kafirci maimakon imani haƙiƙa ya ɓacewa hanyar gaskiya.

(MATSAYIN YAHUDAWA DAGA MUMINAI)

108. Yawaici daga ma'abota Littafi suna gurin su maidaku kafirai bayan imaninku dan hassada daga kawukansu, bayan gaskiya ta bayyana garesu a cikin Attaura (a cikin sha'anin Annabi Sallallahu alaihi wasallama) sai kuyi afuwa ga barinsu, kuyi rangwame; har Allah yazoda al'amarinsa a cikin su (na yaƙi) haƙiƙa Ubangiji Mai ikone shi bisa komai.
109. Ku tsaida salla (zahiri da baɗini), ku bada zakka, duk abinda kuka gabatar ga kawukanku na alhairi (sadaka, ko kyauta) kwa sami sakamakonsa nan ga Allah, haƙiƙa Ubangiji masanine da abinda kuke aikatawa.

(MATSAYIN YAHUDU DA NASARA DANGANE GA WADANSU)

110. Sukace: "Ba wandazai shiga Aljanna sai wanda ya kasance Bayahude, ko Banasare," Wancananka magana; surutansu ne, cene (dasu) "Ku zoda hujjarku inkun kasance magasgata (a cikinta)".
111. Kai! wanda ya miƙa fuskarsa gaba ɗayansa ga Allah, alhali shi yana mai kyakykyawan aiki to, ladansa yana ga Ubangijinsa, ba tsoro a garesu (a duniya) su baza suyi baƙin ciki (a lahira) ba.

وَقَالَتِ الْيَهُودُ لَيْسَتِ النَّصَارَىٰ عَلَىٰ شَيْءٍ وَقَالَتِ النَّصَارَىٰ لَيْسَتِ
الْيَهُودُ عَلَىٰ شَيْءٍ وَهُمْ يَتْلُونَ الْكِتَابَ كَذَٰلِكَ قَالَ الَّذِينَ لَا يَعْلَمُونَ
مِثْلَ قَوْلِهِمْ فَاللَّهُ يَحْكُمُ بَيْنَهُمْ يَوْمَ الْقِيَامَةِ فِيمَا كَانُوا فِيهِ
يَخْتَلِفُونَ ﴿113﴾ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن مَّنَعَ مَسَاجِدَ اللَّهِ أَن يُذْكَرَ
فِيهَا اسْمُهُ وَسَعَىٰ فِي خَرَابِهَا أُولَٰئِكَ مَا كَانَ لَهُمْ
أَن يَدْخُلُوهَا إِلَّا خَائِفِينَ لَهُمْ فِي الدُّنْيَا خِزْيٌ وَلَهُمْ
فِي الْآخِرَةِ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿114﴾ ❋ وَلِلَّهِ الْمَشْرِقُ وَالْمَغْرِبُ ثمن
فَأَيْنَمَا تُوَلُّوا فَثَمَّ وَجْهُ اللَّهِ إِنَّ اللَّهَ وَاسِعٌ عَلِيمٌ ﴿115﴾ وَقَالُوا اتَّخَذَ
اللَّهُ وَلَدًا سُبْحَانَهُ بَل لَّهُ مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ كُلٌّ لَّهُ
قَانِتُونَ ﴿116﴾ بَدِيعُ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ وَإِذَا قَضَىٰ أَمْرًا
فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُ كُن فَيَكُونُ ﴿117﴾ وَقَالَ الَّذِينَ لَا يَعْلَمُونَ
لَوْلَا يُكَلِّمُنَا اللَّهُ أَوْ تَأْتِينَا آيَةٌ كَذَٰلِكَ قَالَ الَّذِينَ
مِن قَبْلِهِم مِّثْلَ قَوْلِهِمْ تَشَابَهَتْ قُلُوبُهُمْ قَدْ بَيَّنَّا
الْآيَاتِ لِقَوْمٍ يُوقِنُونَ ﴿118﴾ إِنَّا أَرْسَلْنَاكَ بِالْحَقِّ
بَشِيرًا وَنَذِيرًا وَلَا تُسْأَلُ عَنْ أَصْحَابِ الْجَحِيمِ ﴿119﴾

112. Yahudu suka ce: "Nasara basu kasance a bisa komai ba," (suka kafirtada Annabi Isa) Nasara sukace "Yahudu basu kasance a bisa komai ba" (suka kafirtada Annabi Musa) alhalin su kuwa suna karanta littafin da aka saukar a garesu, kamar haka wadanda basu da ilmi (mushirikan larabawa da wadansunsu suka fadi irin fadarsu) Ubangiji zaiyi hukunci tsakaninsu ranar alkiyama a cikin abinda suka kasance suna sabani a cikinsa. (Ya shigad da mai gaskiya Aljanna mai karya Wuta).

(RUSA MASALLATAI)

113. Babu mafi zalinci daga wanda ya hana Masallatan Allah a ambaci Allah a cikinta, yayi kokari a cikin rusata (da diga ko wofintarwa) wadancananka bai halatta a garesu shigeta ba, face suna masu jin tsoro, (ai ku tsorata su dayaki kada dayansu ya shige ta yana amintacce) kunyata na garesu a duniya (kisa da ribacewa da jiziya) azaba mai girma na garesu a Lahira.

114. Gabas dayamma sun tabbata ga Allah (ai kasa dukkanta) ko'ina kuka juyad da fuskokinku (a cikin sallah da umarnin Allah) to, cananka ne alkiblar Allah wacce ya yarda da ita, hakika Ubangiji mayalwacin falala ne masanine (dashirin halittarsa).

(KIRKIRE - KIRKIREN AHLIL - KITA-BI DA MUSHIRIKAI)

115. Suka ce: "Ubangiji ya riki da". Tsarki ya tabbata gareshi, bari! abinda yake sammai da kassaina saneda, (mallaka da halittada bauta) dukkan su masu biyayya ne ga Ubangiji.

116. Makagin Sammai da kassai, idan yanufi al-amari sai kawai yace dashi "Samu" saiya samu.

117. Wadanda basu da sani (kafiran Makka) sukace (da Annabi Sallallahu alaihi wasallama) "Danme Allah bai zantad da mu ba (cewa kai Annabinsa ne) ko aya (ta ban mana ki) tazo mana (a bisa gaskiyarka?)" Kamar haka ne wadanda suke gabansu suka fadi (irin maganarsu ga Annabawansu) zukatansu sun kamanci juna (a cikin kafirci da taurin kai) hakika mun bayyana ayoyi ga mutane masu sakankancewa.

(GARGADAR DASHI 'SALLALLAHU ALAHI WASALLAM' DAGA BIN YA-HUDU DA NASARA)

118. Hakika mun aiko ka Annabi (Sallallahu alaihi wasallam) da gaskiya mai albishir (da Aljanna ga wanda ya amsa) mai gargadi (da wuta ga wanda bai amsa ba), kadakai tambayo ga 'yan wuta (danme basu bada gaskiya ba? Iyarwa ne kawai a kanta).

وَلَن تَرْضَىٰ عَنكَ ٱلْيَهُودُ وَلَا ٱلنَّصَٰرَىٰ حَتَّىٰ تَتَّبِعَ مِلَّتَهُمْ
قُلْ إِنَّ هُدَى ٱللَّهِ هُوَ ٱلْهُدَىٰ وَلَئِنِ ٱتَّبَعْتَ أَهْوَآءَهُم بَعْدَ ٱلَّذِے
جَآءَكَ مِنَ ٱلْعِلْمِ مَا لَكَ مِنَ ٱللَّهِ مِن وَلِيٍّ وَلَا نَصِيرٍ ﴿119﴾ ٱلَّذِينَ
ءَاتَيْنَٰهُمُ ٱلْكِتَٰبَ يَتْلُونَهُۥ حَقَّ تِلَاوَتِهِۦٓ أُوْلَٰٓئِكَ يُؤْمِنُونَ بِهِۦ وَمَن يَكْفُرْ بِهِۦ
فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْخَٰسِرُونَ ﴿120﴾ يَٰبَنِےٓ إِسْرَآءِيلَ ٱذْكُرُواْ نِعْمَتِيَ ٱلَّتِےٓ أَنْعَمْتُ
عَلَيْكُمْ وَأَنِّے فَضَّلْتُكُمْ عَلَى ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿121﴾ وَٱتَّقُواْ يَوْمًا لَّا تَجْزِے نَفْسٌ عَن
نَّفْسٍ شَيْـًٔا وَلَا يُقْبَلُ مِنْهَا عَدْلٌ وَلَا تَنفَعُهَا شَفَٰعَةٌ وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ ﴿122﴾
* وَإِذِ ٱبْتَلَىٰٓ إِبْرَٰهِيمَ رَبُّهُۥ بِكَلِمَٰتٍ فَأَتَمَّهُنَّ قَالَ إِنِّے جَاعِلُكَ
لِلنَّاسِ إِمَامًا قَالَ وَمِن ذُرِّيَّتِے قَالَ لَا يَنَالُ عَهْدِے ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿123﴾
وَإِذْ جَعَلْنَا ٱلْبَيْتَ مَثَابَةً لِّلنَّاسِ وَأَمْنًا وَٱتَّخَذُواْ مِن
مَّقَامِ إِبْرَٰهِيمَ مُصَلًّى وَعَهِدْنَآ إِلَىٰٓ إِبْرَٰهِيمَ وَإِسْمَٰعِيلَ
أَن طَهِّرَا بَيْتِيَ لِلطَّآئِفِينَ وَٱلْعَٰكِفِينَ وَٱلرُّكَّعِ ٱلسُّجُودِ ﴿124﴾
وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِيمُ رَبِّ ٱجْعَلْ هَٰذَا بَلَدًا ءَامِنًا وَٱرْزُقْ أَهْلَهُۥ
مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ مَنْ ءَامَنَ مِنْهُم بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ قَالَ وَمَن كَفَرَ
فَأُمْتِعُهُۥ قَلِيلًا ثُمَّ أَضْطَرُّهُۥٓ إِلَىٰ عَذَابِ ٱلنَّارِ وَبِئْسَ ٱلْمَصِيرُ ﴿125﴾

ربع

119. Yahudu da Nasara bazasu yarda dakai ba, sai kaɓi addininsu, cene (dasu) "Haƙiƙa (Musulunci) shine shiriya, (waninsa kuma bata ne)" Wallahi idan kabi soyesoyen zukatansn (takdiran) bayan abinda yazo maka na daga sani (Wahayi) daga Allah, to, baka da wani majibinci dazai kiyaya ka daga Allah, wala mai hana maka azabassa.

120. Waɗannan da muka basu littafi suna karanta shi haƙiƙanin karantawarssa (kamar yadda aka saukar) waɗannan sune suka bada gaskiya dashi (ta sauka a cikin waɗansu jama'a da sukazo daga Habasha suka Musulunta) wanda ya kafirta dashi kuwa, to, waɗancananka sune haƙiƙar taɓaɓɓu.

(GARGADI DA BAN TSORO)

121. Yaku Bani'isra'ila! Ku tuna ni'imata wacce na ni'imta a gareku, kuma haƙiƙa nina fifita ku a kan mutanan (zamanin ku).

122. Kuji tsoron rana wacce wata rai bazata wadatad da komai ga wata rai a cikinta ba, baza a karɓi fansa daga gareta ba, ceto bazata anfaneta ba, kuma su baza a hana musu azabar Allah ba.

(ANNABI IBRAHIMU ALAIHI - ASSALAM DA GINA KA'ABA WANDA YA ƘUNSHI DAWAFI DA RAKA'AUNSA GUDA BIYU DA ADDU'AR ANNABI IBRAHIM GA MAKKATUL MUKARRA-MATI, DA AMINCI DA ALBARKA)

123. (Ka ambata) zamanin da Ubangijin Annabi Ibrahimu ya jarrabe shida kalmomi (umarni da hane - hane) ya badasu cikakku, Ubangiji yace (dashi) "Haƙiƙa ni zan sanya ka abin koyi dashi a cikin addini ga mutane" Annabi yace "Kuma sanya Limana n nan daga 'ya'yayana, "Ubangiji yace: "alƙawarina da Limanci baya samin kafirai".

124. Dayayin da muka sanya ka'aba makoma ga mutane, aminci (daga zalince-zalince da hare-hare), su suka riƙi gurin sallah daga Muƙamin Ibrahima (dutsen daya tsaya a kansa yayin ginin ka'aba ai suke sallar raka biyu ta Dawafi a bayansa) Mun umarci Ibrahimu da Isma'ilu dasu tsarkake ɗakina (daga gumaka), dan masu Dawafi da masuyin ibada a cikinsa da masu ruku'u dasujada a cikinsa. (Ai masu sallah).

125. Da kuma zamanin da Ibrahimu yace: "Ubangiji sanya wannan guri amintacce" (Allah ko ya amsa roƙon Ya sanyashi harami ba a zibda jini na mutum a ciki ba a zaluntar kowa ba a farauta ba a yin ciyawa) Ka azurta mutanensa daga nau'in itatuwa, (shima an amsa da ciro Da'ifa daga Sham izuwa gareshi, da kuma hore arzukan gamuwa izuwa gareta) Wanda yabada gaskiya da Allah daga garesu da ranar Lahira, Ubangiji yace:"Zan azurta wanda ya kafirta ma, to in jiyaddashi dadi mud-dar rayuwarsa, sannan in buƙatar dashi izuwa azabar wuta (a Lahira) tir! Makoma ita".

(ƘANƘANTAR DAKAI GA ALLAH DA ADDU'A)

وَإِذْ يَرْفَعُ إِبْرَاهِيمُ الْقَوَاعِدَ مِنَ الْبَيْتِ وَإِسْمَاعِيلُ رَبَّنَا تَقَبَّلْ مِنَّا
إِنَّكَ أَنتَ السَّمِيعُ الْعَلِيمُ (126) رَبَّنَا وَاجْعَلْنَا مُسْلِمَيْنِ لَكَ
وَمِن ذُرِّيَّتِنَا أُمَّةً مُّسْلِمَةً لَّكَ وَأَرِنَا مَنَاسِكَنَا وَتُبْ عَلَيْنَا
إِنَّكَ أَنتَ التَّوَّابُ الرَّحِيمُ (127) رَبَّنَا وَابْعَثْ فِيهِمْ رَسُولًا مِّنْهُمْ
يَتْلُوا عَلَيْهِمْ ءَايَاتِكَ وَيُعَلِّمُهُمُ الْكِتَابَ وَالْحِكْمَةَ وَيُزَكِّيهِمْ
إِنَّكَ أَنتَ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ (128) وَمَن يَرْغَبُ عَن مِّلَّةِ إِبْرَاهِيمَ
إِلَّا مَن سَفِهَ نَفْسَهُ وَلَقَدِ اصْطَفَيْنَاهُ فِي الدُّنْيَا وَإِنَّهُ فِي الْآخِرَةِ
لَمِنَ الصَّالِحِينَ (129) إِذْ قَالَ لَهُ رَبُّهُ أَسْلِمْ قَالَ أَسْلَمْتُ لِرَبِّ
الْعَالَمِينَ (130) وَأَوْصَىٰ بِهَا إِبْرَاهِيمُ بَنِيهِ وَيَعْقُوبُ يَا بَنِيَّ إِنَّ اللَّهَ
اصْطَفَىٰ لَكُمُ الدِّينَ فَلَا تَمُوتُنَّ إِلَّا وَأَنتُم مُّسْلِمُونَ (131)
* أَمْ كُنتُمْ شُهَدَاءَ إِذْ حَضَرَ يَعْقُوبَ الْمَوْتُ إِذْ قَالَ لِبَنِيهِ
مَا تَعْبُدُونَ مِن بَعْدِي قَالُوا نَعْبُدُ إِلَٰهَكَ وَإِلَٰهَ
ءَابَائِكَ إِبْرَاهِيمَ وَإِسْمَاعِيلَ وَإِسْحَاقَ إِلَٰهًا وَاحِدًا
وَنَحْنُ لَهُ مُسْلِمُونَ (132) تِلْكَ أُمَّةٌ قَدْ خَلَتْ لَهَا مَا كَسَبَتْ
وَلَكُم مَّا كَسَبْتُمْ وَلَا تُسْأَلُونَ عَمَّا كَانُوا يَعْمَلُونَ (133)

ثمن

126. (Ka ambata) zamanin da Annabi Ibrahimu yake ɗaukaka jigajigai na ɗaki da Annabi Isma'ilu (suna cewa) "Ya Ubangijinmu! Karɓi ginin mu daga garemu,haƙiƙa kai kaine mai jin magananmu da aikinmu, masani (dasu).

127. "Ya Ubangijinmu! sanya mu masu jawuwa izuwa gareka, sanya daga 'ya'yanmu jama'a masu jawuwa izuwa gareka, ka sanar da mu shari'ummu da aikin hajjinmu, ka karɓi tubanmu.haƙiƙa kai kaine mai yawan karɓar tuba mai yawan jinƙai.

128. "Ya Ubangijinmu! kuma aiko manzo a cikinsu daga cikinsu, (an amasa,da aiko Annabi S S W)ya dinga karanwan ayoyinka a garesu, yasanad dasu Alkur" ani, da hukunce - hukuncen cikinsa, ya tsarkake su (daga shirka) haƙiƙa kai kaine mai rinjaye gwani (a cikin aiki)".

(ADDININ ANNABI IBRAHIMU DA WANDA YA RATSE MASA)

129. Ba mai ƙyama ga barin addin Annabi Ibrahimu sai wanda ya wautad da kansa, haƙiƙa mun zaɓeshi a duniya (da risala da badaɗantaka) haƙiƙa Annabi Ibrahimu yana cikin managarta a ranar Lahira.

130. Zamanin da Ubangijinsa yace dashi: " Jawu gaba ɗaya,"yace "Na jawu gaba ɗayaga Ubangijin talikai".

131. Annabi Ibrahimu ya wasici 'ya' yansa da Addininsa, da Annabi Yakubu, suka ce: "Yaku 'ya'yana Ubangiji ya zaɓi addinin Musulunci a gareku, kadaku ,mutu face ku Musulmi ne ku".

(RADDI A KAN YAHUDAWA A CIKIN DA'AWAR SU CEWA SU SUNA KAN ADDININ ANNABI IBRAHIMU DA ANNABIYAKUBU)

132. Ko kun kasance mahalarta zamanin da mutuwa ta zowa Yakubu, sandayace da 'ya'yansa "Me zaku bautawa bayan mutuwata?" Suka ce: "Zamu bautawa Ubangijinka, kuma Ubangijin iyayanka, Ibrahimu da Isma'ilu da Ishaka, Ubangiji guda ɗaya, mu masu miƙa dukkanmune a gareshi".

133. Waɗancananka al'umma ce data wuce abindata aikata na gare ta, (na sakamako) ku kuma abinda kuka aikata na gareku baza a tambaye ku ga abinda suka kasance suna aikatawa ba,

وَقَالُواْ كُونُواْ هُودًا أَوْ نَصَٰرَىٰ تَهْتَدُواْ قُلْ بَلْ مِلَّةَ إِبْرَٰهِيمَ
حَنِيفًا وَمَا كَانَ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ (134) قُولُواْ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَمَا أُنزِلَ
إِلَيْنَا وَمَا أُنزِلَ إِلَىٰ إِبْرَٰهِيمَ وَإِسْمَٰعِيلَ وَإِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ وَٱلْأَسْبَاطِ
وَمَا أُوتِيَ مُوسَىٰ وَعِيسَىٰ وَمَا أُوتِيَ ٱلنَّبِيُّونَ مِن رَّبِّهِمْ
لَا نُفَرِّقُ بَيْنَ أَحَدٍ مِّنْهُمْ وَنَحْنُ لَهُۥ مُسْلِمُونَ (135) فَإِنْ ءَامَنُواْ
بِمِثْلِ مَا ءَامَنتُم بِهِۦ فَقَدِ ٱهْتَدَواْ وَّإِن تَوَلَّوْاْ فَإِنَّمَا هُمْ فِي شِقَاقٍ
فَسَيَكْفِيكَهُمُ ٱللَّهُ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْعَلِيمُ (136) صِبْغَةَ ٱللَّهِ
وَمَنْ أَحْسَنُ مِنَ ٱللَّهِ صِبْغَةً وَنَحْنُ لَهُۥ عَٰبِدُونَ (137)
قُلْ أَتُحَآجُّونَنَا فِي ٱللَّهِ وَهُوَ رَبُّنَا وَرَبُّكُمْ وَلَنَا أَعْمَٰلُنَا
وَلَكُمْ أَعْمَٰلُكُمْ وَنَحْنُ لَهُۥ مُخْلِصُونَ (138) أَمْ يَقُولُونَ
إِنَّ إِبْرَٰهِيمَ وَإِسْمَٰعِيلَ وَإِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ وَٱلْأَسْبَاطَ
كَانُواْ هُودًا أَوْ نَصَٰرَىٰ قُلْ ءَأَنتُمْ أَعْلَمُ أَمِ ٱللَّهُ
وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن كَتَمَ شَهَٰدَةً عِندَهُۥ مِنَ ٱللَّهِ وَمَا ٱللَّهُ
بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعْمَلُونَ (139) تِلْكَ أُمَّةٌ قَدْ خَلَتْ لَهَا مَا كَسَبَتْ
وَلَكُم مَّا كَسَبْتُمْ وَلَا تُسْـَٔلُونَ عَمَّا كَانُواْ يَعْمَلُونَ (140)

134. Suka ce: "Ku zamo Yahudu " (inji Yahudawan Madina) ko Nasara (inji Nasaran Najrana) kwa shiriya." Cene dasu, "Kubar wannan magana. zamubi Addinin Annabi Ibrahimu ne, mai fanďarewa addinin ƙarYakuma bai kasance daga Mushirikai ba".

135. Kuce (dasu) "Mun bada gaskiya da Allah da abinda aka saukar a garemu (Ḱur'ani) da abinda aka saukar ga Annabi Ibrahimu (Littattafai guda goma) da Isma'ila, da Ishaka dayakubu da 'ya'yansa, da abinda aka ba Annabi Musa (Attaura) da Isa (Injila) da abinda aka baiwa Annabawa daga Ubangijinsu (Littattafai da Ayoyi) bama rarrabewa tsakanin ɗaya daga garesu, mu masu jawuwa da dukkanmune a gareshi".

136. Idan sun bada gaskiya (Yahudu da Nasara) kamar yadda kuka bada gaskiya dashi haƙiƙa sun shiriya, idan suka juyaga barin bada gaskiya dashi to, su kawai suna cikin saɓanine taredaku, da sannu Ubangiji zai kiyashe ka sharrinsu, shine mai jin (maganganinsu da ayyukansu), masanin (maganganinsu da ayyukansu).

137. Rinin Allah, (ai addininsa wanda ya halicci mutane a kansa saboda bayyanar tasirinsa a bisa mai shi kamar rini a jikin tufa), wanene yafi Allah kyan rini? (babu) mu masu bauta ne a gareshi.

138. Cene (dasu) "danme kuke husuma damu a cikin Allah (dan ya zaɓi Annabi daga Larabawa) shine Ubangijinmu kuma shine Ubangijinku, (yana gareshiya zaɓi wanda yaga dama bayinsa) ayyikanmu na garemu, ku kuma ayyukanku na gareku, za a sakawa kowa abinda ya aikata, mu masu tsarkake addini da aiki ne a gareshi, (mune aulada zaɓi!)".

139. Bari! suna cewa "haƙiƙa Ibrahimu da Isma'ilu da Ishaku, dayakubu da 'ya'yansa sun kasance yahudawa (inji Yahudu) ko Nasara" (inji Nasara) cene (dasu) "Kune masana ko Allah (dayakuɓutad da Annabi Ibrahimu daga waɗannan addinai guda biyu da fadinsa Annabi Ibrahimu bai kasance Bayahude ko Banasare ba?)" Ba mafi zalinci daga wanda ya ɓoye shaidar Allah a wurinsa. (Sune Yahudawa sun ɓoye shaida da Allah yayiwa Annabi Ibrahimu da Hanifanci a cikin Attaura) Allah ba marafkanine ga barin abinda kuke aikatawa ba.

140. Wancananka al'ummace data wuce, abindata aikata na gareta, ku kuma abinda kuka aikata na gareku, baza a tambayeku ga abinda suka kasance suna aikatawa ba.

(LABARTAWA DA GAIBU A CIKIN SHA'ANIN JUYA AL-ḰIBLA)

حزب

* سَيَقُولُ ٱلسُّفَهَآءُ مِنَ ٱلنَّاسِ مَا وَلَّىٰهُمْ عَن قِبْلَتِهِمُ ٱلَّتِي
كَانُواْ عَلَيْهَا قُل لِّلَّهِ ٱلْمَشْرِقُ وَٱلْمَغْرِبُ يَهْدِي مَن يَشَآءُ
إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿141﴾ وَكَذَٰلِكَ جَعَلْنَٰكُمْ أُمَّةً وَسَطًا
لِّتَكُونُواْ شُهَدَآءَ عَلَى ٱلنَّاسِ وَيَكُونَ ٱلرَّسُولُ عَلَيْكُمْ شَهِيدًا
وَمَا جَعَلْنَا ٱلْقِبْلَةَ ٱلَّتِي كُنتَ عَلَيْهَآ إِلَّا لِنَعْلَمَ مَن يَتَّبِعُ
ٱلرَّسُولَ مِمَّن يَنقَلِبُ عَلَىٰ عَقِبَيْهِ وَإِن كَانَتْ لَكَبِيرَةً
إِلَّا عَلَى ٱلَّذِينَ هَدَى ٱللَّهُ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُضِيعَ إِيمَٰنَكُمْ
إِنَّ ٱللَّهَ بِٱلنَّاسِ لَرَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿142﴾ قَدْ نَرَىٰ تَقَلُّبَ وَجْهِكَ
فِي ٱلسَّمَآءِ فَلَنُوَلِّيَنَّكَ قِبْلَةً تَرْضَىٰهَا فَوَلِّ وَجْهَكَ شَطْرَ
ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ وَحَيْثُ مَا كُنتُمْ فَوَلُّواْ وُجُوهَكُمْ شَطْرَهُۥ
وَإِنَّ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلْكِتَٰبَ لَيَعْلَمُونَ أَنَّهُ ٱلْحَقُّ مِن رَّبِّهِمْ
وَمَا ٱللَّهُ بِغَٰفِلٍ عَمَّا يَعْمَلُونَ ﴿143﴾ وَلَئِنْ أَتَيْتَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ
ٱلْكِتَٰبَ بِكُلِّ ءَايَةٍ مَّا تَبِعُواْ قِبْلَتَكَ وَمَآ أَنتَ بِتَابِعٍ قِبْلَتَهُمْ
وَمَا بَعْضُهُم بِتَابِعٍ قِبْلَةَ بَعْضٍ وَلَئِنِ ٱتَّبَعْتَ أَهْوَآءَهُم
مِّنۢ بَعْدِ مَا جَآءَكَ مِنَ ٱلْعِلْمِ إِنَّكَ إِذًا لَّمِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿144﴾

141. Da sannu wawaye na mutane (Yahudu da mushrikai) zasu ce "me ya juyad dasu (Annabi Salallahu alaihi wasallama da muminai) ga barin Al-ƙiblarsu wacce suka kasance a kanta (a cikin salla, Itace Baitil Maƙadisi?)" cene (dasu) "Gabas dayamma (ai juhohi dukkansu na Allah ne (Sai yai umarni da fiskantar kowace jiha yaga dama ba mai cewa dan me) Yana. shiriyar (wanda yaga damar shiriyarsa) izuwa tafarki madaidaici. (Addinin musulunci, ai ku kuna daga cikinsu)".

142. Haka nan kamar da muka shirye ku izuwa gareshi muka sanya ku (YA UMMATA MUHAMMADIN al'umma zaɓaɓɓu, adalai dan ku zamo shaida bisa mutane (ranar al-ƙiyama cewa Manzanni sun zo musu) kuma Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) ya kasance shaida a kanku, (cewa ya iyar muku) bamu sanya al-ƙiblar da kake kantada farko (Itace Ka'aba) al-ƙiblar ka a yanzu ba, sai dai dan mu nuna wanda yake bin manzan Allah (Sallallahu alaihi wasallama yagasgata shi) daga wanda yake juyawa a kan digadigansa, (izuwa kafirci) haƙiƙa juyawan nan izuwa gareta ya kasance mai nauyi a bisa mutane sai ga waɗanda Allah ya shiriya daga garesu, Allah bazai tozarta sallarku izuwa Baitil Maƙadisi ba, zaiyi muku sakamako a kanta, Ubangiji mai tsananin jinƙaine da rahama ga Mumunai.

JUYAR DA AL-ƘIBLA IZUWA KA'ABA)

143. Haƙiƙa muna ganin juyawar fuskarka a cikin jihar sama (dan bege izuwa Wahayi) to, Wallahi zamu fuskantar dakai al-ƙibla da kake yarda da ita, to, juyar da fuskarka (a cikin sallah) katarnin masallaci mai alfarma (ka'aba) a inda, duk kuke (Ya al'ummar Annabi) to, ku juyar da fuskokinku (a cikin sallah) katarninta, Haƙiƙa Waɗanda aka basu Littafi lallai sunsan Haƙiƙa juyawa izuwa Ka'abashine gaskiya daga Ubangijinsu, (saboda abinda yake cikin Littafinsu na kwatanta Annabi Sallalla-hu alaihi wasallama da juyawa izuwa gareta), Ubangiji ba marabkani bane ga barin abinda suke aikatawa.

144. Wallahi idan kazowa waɗanda aka basu Littafi da kowace aya (a kan gaskiyar ka a cikin al'amarin al-ƙibla,) bazasu bi al-ƙiblarka ba (dan taurin kai), kai bazaka bi al-ƙiblarsu ba (dan bazasu Musulunta ba har abada bakuma zaka koma izuwa Al-ƙiblarsu) ba, ba'alinsu ba mai bin al-ƙiblar ba'ali bane (ai Yahudu bazasu bi al-ƙiblar Nasara ba, kazalika Nasara bazasu bi ta Yahudu ba), Wallahi idan kabi soyesoyen zikatansu (wacce suke kiranka zuwa gareta) bayan abinda yazo maka (na daga wahayi,) haƙiƙa kai (in kabi su takdiri) hakika kana a cikin azzalimai.

ٱلَّذِينَ ءَاتَيْنَٰهُمُ ٱلْكِتَٰبَ يَعْرِفُونَهُۥ كَمَا يَعْرِفُونَ أَبْنَآءَهُمْ وَإِنَّ فَرِيقًا
مِّنْهُمْ لَيَكْتُمُونَ ٱلْحَقَّ وَهُمْ يَعْلَمُونَ ﴿145﴾ ٱلْحَقُّ مِن رَّبِّكَ فَلَا تَكُونَنَّ
مِنَ ٱلْمُمْتَرِينَ ﴿146﴾ * وَلِكُلٍّ وِجْهَةٌ هُوَ مُوَلِّيهَا فَاسْتَبِقُواْ ٱلْخَيْرَٰتِ ثمن
أَيْنَ مَا تَكُونُواْ يَأْتِ بِكُمُ ٱللَّهُ جَمِيعًا إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ
كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ﴿147﴾ وَمِنْ حَيْثُ خَرَجْتَ فَوَلِّ وَجْهَكَ
شَطْرَ ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ وَإِنَّهُۥ لَلْحَقُّ مِن رَّبِّكَ وَمَا ٱللَّهُ
بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعْمَلُونَ ﴿148﴾ وَمِنْ حَيْثُ خَرَجْتَ فَوَلِّ وَجْهَكَ
شَطْرَ ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ وَحَيْثُ مَا كُنتُمْ فَوَلُّواْ وُجُوهَكُمْ شَطْرَهُۥ
لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَيْكُمْ حُجَّةٌ إِلَّا ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ
مِنْهُمْ فَلَا تَخْشَوْهُمْ وَٱخْشَوْنِي وَلِأُتِمَّ نِعْمَتِي عَلَيْكُمْ
وَلَعَلَّكُمْ تَهْتَدُونَ ﴿149﴾ كَمَا أَرْسَلْنَا فِيكُمْ رَسُولًا مِّنكُمْ
يَتْلُواْ عَلَيْكُمْ ءَايَٰتِنَا وَيُزَكِّيكُمْ وَيُعَلِّمُكُمُ ٱلْكِتَٰبَ
وَٱلْحِكْمَةَ وَيُعَلِّمُكُم مَّا لَمْ تَكُونُواْ تَعْلَمُونَ ﴿150﴾ فَٱذْكُرُونِي
أَذْكُرْكُمْ وَٱشْكُرُواْ لِي وَلَا تَكْفُرُونِ ﴿151﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ ٱسْتَعِينُواْ بِٱلصَّبْرِ وَٱلصَّلَوٰةِ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ﴿152﴾

145. Wađanda muka basu Littafi sunsan Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) tamfad da sukasan 'ya'yansu (saboda kamanninsa a cikin Littattafansu) haƙiƙa wađansu jama'a daga cikinsu suna ɓoyewan gaskiya (kamar kamannin Annabi Sallallahu alaihi wasallama) alhali sunsan (kaine wanda aka ambata a cikin littafinsu).

146. Gaskıya daga Ubangijinka take, to, fa kadaka zamo daga masu kokwanto (a cikinta).

(WANI ABU DAGA AIKIN SHA'ANIN JUYA AL-ƘIBLA)

147. Kowace al'umma tana da al-ƙibla da take fiskantatta a cikin sallah, sai kuyi tsane zuwa aikin da'o'i, inda duk kuka kasance Allah zai taraku baki daya ranar Alƙiyama don sakamako, haƙiƙa Ubangiji mai ikone bisa komai.

148. Daga inda duk Kafita (saboda tafiya) to ka juyad da fuskarka katarnin masallaci mai alfarma, haƙiƙa shi juyawan nan shine gaskiya daga Ubangijinka, Allah ba marabkanine ga barin abinda kuke aikatawa ba.

149. Daga duk indaka fita, to, juyad da fuskarka katarnin masallaci mai alfarma, a inda duk kuka kasance, to, ku juyad da fuskokinku katarinsa (an maimaita saboda karfafawa) dai kada hujja ga mutane ta kasance a kanku (Yahudu ko Mushrikai) sai wađandasu ka zalinci daga garesu (da taurin kai) to, kada kuji tsoronsu, kuji tsoro na, kuma dan in cika ni'imata a gareku (dashirya daku zuwa alamomin addininku), kuma dan haƙiƙa ku sami shiriya zuwa gaskiya.

150. (Cikawar ni'ima) kamar (irin cikawar ni'imar) da muka mukuda aiko Annabi daga cikinku a cikinku (shine Annabi Sallallahu alaihi wasallama) da yake karantawar ayoyina a gareku, yake tsarkake ku daga shirka, yake sanar daku Alƙur'ani da hukunce - hukuncen cikinsa, yake sanar daku abinda baku kasance kun saniba.

151. Ku ambaceni, na ambace ku (a cikin Hadisi ƙudisi, wanda ya ambaceni a cikin kansa, na ambace shi a cikin kaina, wanda ya ambace ni a cikin jama'a, na ambace shi a cikin jama'ar datafi jama'arsa). Kuyi godiyagareni (da đa'a), kadaku ,bitilce mini (da saɓo).

(MASU HAƘURI DA MASU YAƘI SABODA INGANTA ADDININ ALLAH)

152. Yaku wađanda kuka bada gaskiya! ku nemi taimako (a kan Lahira) da haƙuri (bisa đa'a da bala'i ku nemi taimako) da sallah, haƙiƙa Ubangiji yana tareda masu haƙuri (da taimako).

وَلَا تَقُولُوا لِمَن يُقْتَلُ فِي سَبِيلِ اللَّهِ أَمْوَاتٌ بَلْ أَحْيَاءٌ
وَلَٰكِن لَّا تَشْعُرُونَ (153) وَلَنَبْلُوَنَّكُم بِشَيْءٍ مِّنَ الْخَوْفِ وَالْجُوعِ
وَنَقْصٍ مِّنَ الْأَمْوَالِ وَالْأَنفُسِ وَالثَّمَرَاتِ وَبَشِّرِ الصَّابِرِينَ (154)
الَّذِينَ إِذَا أَصَابَتْهُم مُّصِيبَةٌ قَالُوا إِنَّا لِلَّهِ وَإِنَّا إِلَيْهِ رَاجِعُونَ (155)
أُولَٰئِكَ عَلَيْهِمْ صَلَوَاتٌ مِّن رَّبِّهِمْ وَرَحْمَةٌ وَأُولَٰئِكَ هُمُ الْمُهْتَدُونَ (156)
ربع * إِنَّ الصَّفَا وَالْمَرْوَةَ مِن شَعَائِرِ اللَّهِ فَمَنْ حَجَّ الْبَيْتَ أَوِ اعْتَمَرَ
فَلَا جُنَاحَ عَلَيْهِ أَن يَطَّوَّفَ بِهِمَا وَمَن تَطَوَّعَ خَيْرًا
فَإِنَّ اللَّهَ شَاكِرٌ عَلِيمٌ (157) إِنَّ الَّذِينَ يَكْتُمُونَ مَا أَنزَلْنَا مِنَ
الْبَيِّنَاتِ وَالْهُدَىٰ مِن بَعْدِ مَا بَيَّنَّاهُ لِلنَّاسِ فِي الْكِتَابِ
أُولَٰئِكَ يَلْعَنُهُمُ اللَّهُ وَيَلْعَنُهُمُ اللَّاعِنُونَ (158) إِلَّا الَّذِينَ تَابُوا
وَأَصْلَحُوا وَبَيَّنُوا فَأُولَٰئِكَ أَتُوبُ عَلَيْهِمْ
وَأَنَا التَّوَّابُ الرَّحِيمُ (159) إِنَّ الَّذِينَ كَفَرُوا وَمَاتُوا وَهُمْ كُفَّارٌ
أُولَٰئِكَ عَلَيْهِمْ لَعْنَةُ اللَّهِ وَالْمَلَائِكَةِ وَالنَّاسِ أَجْمَعِينَ (160)
خَالِدِينَ فِيهَا لَا يُخَفَّفُ عَنْهُمُ الْعَذَابُ وَلَا هُمْ يُنظَرُونَ (161)
وَإِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَاحِدٌ لَّا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ الرَّحْمَٰنُ الرَّحِيمُ (162)

153. Kadaku ,fada ga wadanda aka kashe su saboda Allah su matattu ne, a'a su rayayyu ne (rayukan su suna cikin maroran tsintsaye kwarra tana yawo a cikin Aljanna inda duk ta ga dama) amma baku san abinda suke ciki ba, (idandinan ku basa ganin' abinda suke ciki).

154. Wallahi zamu jarrabe kuda wani abu na tsoro (daga abokan gaba), da fari da tawayar dukiyoyi, da kawuka (kisa, mutuwa, cuce-cuce, binne 'ya'ya da satar 'ya'ya) da 'ya'yan itatuwa (kamar wabi), yiwa masu dauriya (sa kan bala'i) albishir (da Aljanna).

155. Sune wadanda idan musibata samesu sukance "Muna Allah ne (mallaka, da halitta, dabauta) hakika mu masu komawa ne zuwa gareshi (a ranar Lahira dan sakamako).

156. Wadancananka gafara daga Ubangijinsu ta tabbata a garesu da jinkai, wadancananka sune cikakkun masu shiriya.

(WANI ABU DAGA ALAMOMIN HAJJI, DA SAKAMAKON WANDA YA BOYE AYOYIN ALLAH)

157. Hakika dutsan Safa da dutsan Marwa suna daga alamomin Addinin Allah, wanda yayi niyar Hajji ko Umra ba laifi gareshi yayi sa'ayi a tsakaninsu, wanda yayi taduwu'a na alhairi, to, hakika Allah mai godewane (a gareshi) masanine (dashi).

158. Hakika wadannan dasuke boyewar abinda muka saukar na daga hujjoji dashiriya (kamar ayatirrajami da kamannin Annabi Sallallahu alaihi wasallama) bayan mun bayyana shi ga mutane a cikin Attaura, wancananka Allah yana tsine musu albarka, kuma masu tsinewa (Mala'ikuda Muminai da kowane abu) suna tsine musu albarka.

159. Sai wadanda suka tubasukayi aiki na gari suka bayyana abinda suka boye, to, wadancananka ina karbar tubansu, nine mai yawan karbar tuba, mai yawan jinkai (ga muminai).

160. Hakika wadannan da suka kafirta suka mutu suna kafirai, wadancananka la'anar Allah na garesu da Mala'ikuda mutane baki daya.

161. Masu dauwama a cikin (azabar) la'anar ba a sauwake azabar ga barin su, (koda kiftawar ido) baza ayi musu sauraro (dan su tuba ba).

(TABBATAR DA KADAITAKAR ALLAH DA RAHAMARSA)

162. Ubangijinku Ubangiji ne guda daya (bashida Kini a cikin Zatinsa, ko sifofinsa, ko aikinsa), babu abin bautawa da gaskiya. saishi, mai jinkan talikai a duniya baki daya, Mai jinkan muminai a Lahira a kebe.

إِنَّ فِي خَلْقِ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَاخْتِلَافِ الَّيْلِ وَالنَّهَارِ
وَالْفُلْكِ الَّتِي تَجْرِي فِي الْبَحْرِ بِمَا يَنفَعُ النَّاسَ وَمَا أَنزَلَ
اللَّهُ مِنَ السَّمَاءِ مِن مَّاءٍ فَأَحْيَا بِهِ الْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَا
وَبَثَّ فِيهَا مِن كُلِّ دَابَّةٍ وَتَصْرِيفِ الرِّيَٰحِ وَالسَّحَابِ
الْمُسَخَّرِ بَيْنَ السَّمَاءِ وَالْأَرْضِ لَآيَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَعْقِلُونَ ﴿163﴾
وَمِنَ النَّاسِ مَن يَتَّخِذُ مِن دُونِ اللَّهِ أَندَادًا يُحِبُّونَهُمْ كَحُبِّ اللَّهِ
وَالَّذِينَ ءَامَنُوا أَشَدُّ حُبًّا لِّلَّهِ وَلَوْ يَرَى الَّذِينَ ظَلَمُوا
إِذْ يَرَوْنَ الْعَذَابَ أَنَّ الْقُوَّةَ لِلَّهِ جَمِيعًا وَأَنَّ اللَّهَ شَدِيدُ
الْعَذَابِ ﴿164﴾ إِذْ تَبَرَّأَ الَّذِينَ اتُّبِعُوا مِنَ الَّذِينَ اتَّبَعُوا
وَرَأَوُا الْعَذَابَ وَتَقَطَّعَتْ بِهِمُ الْأَسْبَابُ ﴿165﴾ وَقَالَ الَّذِينَ اتَّبَعُوا
لَوْ أَنَّ لَنَا كَرَّةً فَنَتَبَرَّأَ مِنْهُمْ كَمَا تَبَرَّءُوا مِنَّا كَذَٰلِكَ يُرِيهِمُ اللَّهُ
أَعْمَالَهُمْ حَسَرَٰتٍ عَلَيْهِمْ وَمَا هُم بِخَٰرِجِينَ مِنَ النَّارِ ﴿166﴾
* يَٰأَيُّهَا النَّاسُ كُلُوا مِمَّا فِي الْأَرْضِ حَلَٰلًا طَيِّبًا وَلَا تَتَّبِعُوا
خُطُوَٰتِ الشَّيْطَٰنِ إِنَّهُ لَكُمْ عَدُوٌّ مُّبِينٌ ﴿167﴾ إِنَّمَا يَأْمُرُكُم
بِالسُّوءِ وَالْفَحْشَاءِ وَأَن تَقُولُوا عَلَى اللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿168﴾

ثمن

163. Hakika akwai ayoyi (masu nuna dayantakar Allah) a cikin halittar sammai da kassai (da abinda yake cikinsu na mana ki) haka ma akwai a cikin kaikawon dare da rana (ta wajen karuwa da rayuwa) haka ma akwai a cikin jiraga dasuke gudana a cikin kogi (ba taredasun nitse ba) suna jinkire da abinda yake amfanin mutane (na cineke-cineke da lafce-lafcen fasinja da waninsu) akwai a cikin abinda Allah ya saukar daga sama shine ruwa ya raya kasa dashi (da tsiri) bayan ta kekashe, ya daidaita a cikinta daga nau'in dukkan mai motsi a bayan kasa akwai a cikin jujjuyawan nan na iskoki (dama da hagun, zafi da sanyi kuma) akwai a cikin girgije abin horewa (daga Allah, yana tafiya inda Allah yaso) tsakanin sama da kasa (bada wani abinda ya rike shi ba) ga mutane masu amfani da hankalinsu.

(HALIN MUSHRIKAI TAREDA IYAYEN - GIJINSU A DUNIYA DA LAHIRA)

164. Akwai daga mutane wanda yake rikon gumaka ba Allah ba, suna sonsu (da girmama wa da kankan da kai) kamar sonsu ga Allah, wadanda suka bada gaskiya sun fi tsananin so ga Allah (daga suda gumakansu dan muminai suna tareda Allah a kowane hali), da kana ganin wadandasu kayi zalinci (da bautar gumaka) zamanin dasuke ganin azaba (da kaga al'amari mai girma) dan hakika karfi ya tabbata ga Allah baki daya, kuma dan hakika Allah mai tsananin azaba ne.

165. Yayin da wadanda aka bisu (shuwagabanni) suke kubuta daga wadanda suka bisu, alhali hakika sun ga azaba, a lokacin da sabubban jinkai ta yanke ga barinsu.

166. Wadanda sukabi sukace: Inama muna da komowa (zuma duniya) mu kubuta daga shuwagabannin nan, kamar da suka kubuta daga garemu (a Yau?) Kamar yandaya nuna musu tsananin azabarsa da kubutar ba'alinsu daga ba'ali, Allah yake nuna musu miyagun ayyukansu, nadamce-nadamce a garesu, su bazasu fita daga wuta ba, (bayan shigar ta).

(WANI ABU DAGA MAGANTAR MASU ROKON ABABAN BAUTAWA BA ALLAH BA)

167. Yaku jama'ar Annabi (Sallallahu alaihi wasallama!) Kuci daga abinda yake cikin kasa halali daddada, kada kubi kawace - kawacen shaidan, hakika shi magauci ne mabayyanin kiyayya a gareku.

168. Shi kawai yana umarninkune da aikin zinibi, da aikin ashsha da kuma ku kagawa Allah abinda baku san (hukuncinsa ba).

وإذا قيل لهم اتبعوا ما أنزل الله قالوا بل نتبع ما ألفينا
عليه آباءنا أولو كان آباؤهم لا يعقلون شيئا
ولا يهتدون ﴿169﴾ ومثل الذين كفروا كمثل الذي ينعق
بما لا يسمع إلا دعاء ونداء صم بكم عمي فهم لا يعقلون ﴿170﴾
يا أيها الذين آمنوا كلوا من طيبات ما رزقناكم واشكروا لله
إن كنتم إياه تعبدون ﴿171﴾ إنما حرم عليكم الميتة
والدم ولحم الخنزير وما أهل به لغير الله فمن اضطر
غير باغ ولا عاد فلا إثم عليه إن الله غفور رحيم ﴿172﴾
إن الذين يكتمون ما أنزل الله من الكتاب
ويشترون به ثمنا قليلا أولئك ما يأكلون
في بطونهم إلا النار ولا يكلمهم الله يوم القيامة
ولا يزكيهم ولهم عذاب أليم ﴿173﴾ أولئك الذين اشتروا
الضلالة بالهدى والعذاب بالمغفرة فما أصبرهم
على النار ﴿174﴾ ذلك بأن الله نزل الكتاب بالحق
وإن الذين اختلفوا في الكتاب لفي شقاق بعيد ﴿175﴾

169. Idan ance da kafirai: "Kubi abinda Allah ya saukar (na tauhidi da halatta halal, da waninsa)" sai suce: "A'a, bari! zamubi abinda muka sami iyayanmu a kansa, (bautar gunki da nonan gunki [1] da bayansa [2] Ubangiji yace): "Sa dinga bin su koda iyayen nan nasu sun kasance basa hankaltar komai (na sha'anin addini) basa shiriya (zuwa gaskiya?").

170. Misalin waɗanda suka kafirta (da wanda yake kiransu zuwa shiriya) kamar wanda yake murya da abinda bayajin komai, sai tsikaye wato yafucc da kira (muryar da baya fahimtar ma'anarta), su kurame ne be-baye ne makafi ne basa fahimtar (gargaɗi).

(HALAL DA HARAM A CIKIN ABINCI)

171. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya! kuci daga halaliyar abinda muka azurta muku, ku godewa Allah a bisa abinda ya halatta muku in kun kasance shi kaɗai ku ke bautawa.

172. Haƙiƙa Ubangiji; mushe kaɗai ya haramta mukuda jini (na hadahu, ai wanda yake fita da wanda yake shiga cikin dabba) da naman alhanzir da abinda aka kummta wani suna yayin yankansa bana Allah ba, to, wanda larura ta tilarta shi yaci wani abu daga abinda aka ambata ba yana ɗan tawaye ba, ba ɗan fashi ba, to, ba laifi a gareshi, haƙiƙa Ubangiji mai yawan gafara ne mai yawan jinƙai(ga muminai).


(MATSAYIN AHLIL - KITABI DAGA AL-ƘUR'ANI DA ANNABI SALLALLA-HU ALAIHI WASALLAMA)

173. Waɗannan dasuke ɓoye abinda Allah ya saukar na daga Littafi (kamannin Annabi Sallallahu alaihi wasallama, sune Yahudu) suke musanyo ɗan tamani ƙanƙani maimakonsa, waɗancananka basa cin komai a cikin cikkunansu sai wuta (dan Itace makomarsu) Allah bazai zance dasu ba ranar Al-ƙiyama (dan fushi a garesu) Allah bazai shaida da tsarki daga zunubai a garesu ba, azaba mai raɗaɗi tana garesu.

174. Waɗancananka ne waɗanda suka sai ɓata dashiriya a duniya, suka sai azabada gafara (a Lahira da basu ɓoye ba) Mana kin abinda ya haƙurƙurtar dasu akan wuta!.

175. Wancananka (abinda aka ambata shiga wutada waninsa) saboda haƙiƙa Allah ya saukar da littafi da gaskiya sukai saɓani daban-daban a cikinsa, haƙiƙa waɗanda sukai daban-daban a cikin littafi (Attaura da Alƙur'ani) lallai suna cikin saɓani mai nisa ga barin gaskiya.

1) wato bazasu sha nonon wannan taguwa ba sa-bodata gunkica.
2) bazasu hau wannan taguwa bazasu dora masa kaya sabodata gunke ce.



۞ لَّيْسَ اَلْبِرَّ أَن تُوَلُّواْ وُجُوهَكُمْ قِبَلَ اَلْمَشْرِقِ وَالْمَغْرِبِۖ
وَلَٰكِنِ اِلْبِرُّ مَنْ ءَامَنَ بِاللَّهِ وَالْيَوْمِ اِلْأٓخِرِ وَالْمَلَٰٓئِكَةِ
وَالْكِتَٰبِ وَالنَّبِيٓـِٔينَ وَءَاتَى اَلْمَالَ عَلَىٰ حُبِّهِۦ ذَوِے اِلْقُرْبَىٰ
وَالْيَتَٰمَىٰ وَالْمَسَٰكِينَ وَابْنَ اَلسَّبِيلِ وَالسَّآئِلِينَ وَفِے اِلرِّقَابِ
وَأَقَامَ اَلصَّلَوٰةَ وَءَاتَى اَلزَّكَوٰةَۖ وَالْمُوفُونَ بِعَهْدِهِمُۥٓ إِذَا عَٰهَدُواْۖ
وَالصَّٰبِرِينَ فِے اِلْبَأْسَآءِ وَالضَّرَّآءِ وَحِينَ اَلْبَأْسِۖ أُوْلَٰٓئِكَ اَلَّذِينَ
صَدَقُواْۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ اُلْمُتَّقُونَۖ (176) يَٰٓأَيُّهَا اَلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُتِبَ
عَلَيْكُمُ اُلْقِصَاصُ فِے اِلْقَتْلَىۖ اَلْحُرُّ بِالْحُرِّ وَالْعَبْدُ بِالْعَبْدِ وَالْأُنثَىٰ
بِالْأُنثَىٰۖ فَمَنْ عُفِيَ لَهُۥ مِنْ أَخِيهِ شَےْءٞ فَاتِّبَاعُۢ بِالْمَعْرُوفِ وَأَدَآءٌ
إِلَيْهِ بِإِحْسَٰنٖۖ ذَٰلِكَ تَخْفِيفٞ مِّن رَّبِّكُمْ وَرَحْمَةٞۖ فَمَنِ اِعْتَدَىٰ
بَعْدَ ذَٰلِكَ فَلَهُۥ عَذَابٌ أَلِيمٞۖ (177) وَلَكُمْ فِے اِلْقِصَاصِ حَيَوٰةٞ يَٰٓأُوْلِے
اِلْأَلْبَٰبِ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَۖ (178) كُتِبَ عَلَيْكُمُۥٓ إِذَا حَضَرَ
أَحَدَكُمُ اُلْمَوْتُ إِن تَرَكَ خَيْرًا اِلْوَصِيَّةُ لِلْوَٰلِدَيْنِ وَالْأَقْرَبِينَ
بِالْمَعْرُوفِۖ حَقًّا عَلَى اَلْمُتَّقِينَۖ (179) فَمَنۢ بَدَّلَهُۥ بَعْدَ مَا سَمِعَهُۥ
فَإِنَّمَآ إِثْمُهُۥ عَلَى اَلَّذِينَ يُبَدِّلُونَهُۥٓۖ إِنَّ اَللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٞۖ (180)

(HAƘIƘAR AIKIN KIRKI)

176. Ku juyar da fuskokinku a cikin sallah katarnin mahudar rana da mafaɗar ta bashine aikin kirki ba (raddi ne kan Yahudu da Nasara da suka riya haka) kai dai wanda ya bada gaskiya da Allah da ranar Lahira, da Mala'ikuda Littattafai Basamawiyai da Annabawa, ya bada dukiya tareda san dukiyan nan ga ma'abota ziminci yaba marayu da miski-nai da ɗan tafarki, da mabarata, kuma ya bayar a cikin wabo wuyayu (ai fanso su) ya tsaida sallah (da haƙƙoƙinta na zahiri dana baɗini) ya bada zakka ta farilla, da masu cikawa da al-ƙawarinsu idan sun yiwa Allah al-ƙawari ko mutane, (waɗannan sune masu aikin kirki), ina kirari ga masu haƙuri a cikin tsananin talauci, da rashin lafiya, da lokacin tsanantar yaƙi saboda Allah, waɗancananka sune waɗanda suka gasgata (a cikin imani da aikin kirki), kuma wadancananka sune haƙiƙar masu tsoron Allah.

(ƘISASI DA AMFANINSA)

177. Ya waɗanda kuka bada gaskiya! an wajabta daidaitawa a gareku a cikin ƙasassu, da ana kashe shi saboda kisan da, (baza a kashe shi saboda bawa ba). Bawa ana kashe shi saboda kisan Bawa, mace ana kashe ta saboda kisan mace, kuma ana kashe namiji saboda kashe ta, (wannan daidaito ana Kula dashi ta wajen addini, baza a kashe Musulmi ba koda Bawa ne saboda kafiri koda ɗane) wanda akayi masa rangwamen wani abu daga jinin ɗan uwansa (abin kashewa, aka bar ƙisasi,) to, shi mai afuwa bine a gareshi ga mai kisa da abin sani a shari'a (ya neme shi da diyya bada tsanani ba,) kuma mika diyyaga mai rangwami yana kan mai kisa bada taurin bashi ba, da ragewa, wancananka (hukunci, ƙisasi da rangwami da karɓar diyya) sawwaƙewa ne daga Ubangijinkuda rahama a gareku (bakamar Yahudu da aka wajabta musu ƙisasi ko Nasara da aka wajabta musu diyya ba) wanda yai shishshigi da kashe mai kisa bayan wancanaka (afuwa,) to, azaba mai raɗaɗi ta tabbata a gareshi (a duniya da lahira wato kisa dashiga wuta).

178. Kuna da rayuwa mai girma a cikin ƙisasi ya ma'abota hankula, (domin mai kisa idan yasan za a kashe shi saiya tsautu ya raya kansa da wanda yayi nufin ya kashe, saboda haka aka wajabta shi) dan ku tsoraci kisa saboda tsoron sakayya.

(WASIYYA)

179. Ubangiji ya wajabta wasiyya a gareku, idan sabubban mutuwa ta halarci ɗayanku in yabar dukiya, to, yayi wasiyyaga iyayansa da. mafi kusanci dashi da abin sani a shari'a (kada ya ƙara kan sulusi kada ya fifita mawadaci) Allah ya tabbatar da wannan tabbatarwa ga masu jin tsoron Allah. (wannan shafaffe ne da ayar gado, da kuma Hadisin ba wasiyyaga magaji wanda Tirmizi ya ruwaito).

180. To, duk wanda ya musanya wannan wasiyya (shaida ne ko wasiyyi) bayan yasanshi, to, kawai zunibinsa yana kan waɗanda suka musanyashi Ubangiji mai jine (ga maganar kowa da aikinsa,) masanine (da maganar kowa da aikinsa).

فَمَنْ خَافَ مِن مُّوصٍ جَنَفاً اَوْ اِثْماً فَأَصْلَحَ بَيْنَهُمْ
فَلَا إِثْمَ عَلَيْهِ إِنَّ اللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿181﴾ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ
ءَامَنُوا كُتِبَ عَلَيْكُمُ الصِّيَامُ كَمَا كُتِبَ عَلَى الَّذِينَ
مِن قَبْلِكُمْ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴿182﴾ أَيَّاماً مَّعْدُودَاتٍ فَمَن كَانَ
مِنكُم مَّرِيضاً اَوْ عَلَىٰ سَفَرٍ فَعِدَّةٌ مِّنْ أَيَّامٍ اُخَرَ وَعَلَى الَّذِينَ
يُطِيقُونَهُ فِدْيَةٌ طَعَامِ مَسَاكِينَ فَمَن تَطَوَّعَ خَيْراً فَهْوَ خَيْرٌ لَّهُ
وَأَن تَصُومُوا خَيْرٌ لَّكُمْ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿183﴾ * شَهْرُ
رَمَضَانَ الَّذِي أُنزِلَ فِيهِ الْقُرْءَانُ هُدًى لِّلنَّاسِ
وَبَيِّنَاتٍ مِّنَ الْهُدَىٰ وَالْفُرْقَانِ فَمَن شَهِدَ مِنكُمُ
الشَّهْرَ فَلْيَصُمْهُ وَمَن كَانَ مَرِيضاً اَوْ عَلَىٰ سَفَرٍ فَعِدَّةٌ
مِّنْ أَيَّامٍ اُخَرَ يُرِيدُ اللَّهُ بِكُمُ الْيُسْرَ وَلَا يُرِيدُ بِكُمُ
الْعُسْرَ وَلِتُكْمِلُوا الْعِدَّةَ وَلِتُكَبِّرُوا اللَّهَ عَلَىٰ مَا هَدَاكُمْ
وَلَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿184﴾ وَإِذَا سَأَلَكَ عِبَادِي عَنِّي
فَإِنِّي قَرِيبٌ اُجِيبُ دَعْوَةَ الدَّاعِ إِذَا دَعَانِ
فَلْيَسْتَجِيبُوا لِي وَلْيُؤْمِنُوا بِي لَعَلَّهُمْ يَرْشُدُونَ ﴿185﴾

ثمن

181. To, duka wanda yaji tsoron ratsewa ga barin gaskiya daga mai wasiyya da kuskure, ko kuma ratsewa da gangan ko (ƙari kan sulusi ko fifita mawadaci, saboda haka ya gyara a tsakaninsu (Mai wasiyya da abin yiwa wasiyya, ya umarce su da adalci) to babu laifi a gareshi (cikin wannan) haƙiƙa Ubangiji mai yawan gafara ne mai jinƙai.

(AZUMI DA WAJABCINSA)

182. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya! an wajabta azumi a gareku, tamfad da aka wajabta shi bisa ga waɗanda suke gaban ku na daga al'umma, dan hakika ku tsoraci Allah.

183. Kwananaki kaɗan ababan ƙirgawa (Ramalanu) to, duk wanda 'ya kasance marar lafiya daga cikinku (yayin ganinsa) ko yake bisa tafiya (azumi zai wahalda dashi) to, gwargwadon abinda yaci na daga kwanika waɗansu (yana kansa,) fidya tana kan waɗanda suke da iko yin azumi tareda wahala (Itace) abincin miskinai (ai gwargwadon abinda mutum zai ci a wuninsa shine mudu ɗaya daga marmjayin abincin gari ga kowace rana) duka wanda yai tadauwu'a na alhairi (ya kara kan gwargwadon da aka ambata a fidya) to, (karin nan),shi yafi alhairi a gareshi, kuyi azumi shi yafi amfani a gareku (ai ku daure kuyi azumi yafi Kuci kuyi fidya) ir kun kasance kun san (haka ye fi to, ku aikata shi).

184. Watan Ramalanu shine wanda aka saukad da Alƙur'ani a cikinsa (daga Lauhul - Mahfuzu zuwa sama ta duniya a Lailatil -(ƙadari) mai shiriyad (da mutane daga ɓata,) ayoyi mabayyana na shiriya (zuwa hukuncin gaskiya) na rarrabewa (tsakanin ƙarya da gaskiya,) dukawanda yaga wata daga cikinku to, ya azimce shi, wanda ya kasance marar lafiyako a kan tafiya to, gwargwadon abinda yaci (yana kansa) na daga kwanika waɗansu, Allah yana nufin sauki daku ,baya nufin tsanani da ku, (saboda haka ya halatta muku shan azumi a cikin rashin lafiya da tafiya,) kuma dan ku cika ƙirgar (azu-min Ramalanu) kuma dan ku girmama Allah (yayin cikatta a ranar Idi, shine ku ce'Allahu Akbar, Allahu Akbar), saboda ya shirye ku (ga alamomin Addininsa,) kuma dan hakika ku gode (masa wannan ni'ima).

(MURAKABAR UBANGIJI SUBHANA-HU WA TA'ALA)

185. Idan bayina sun tambaye ka gareni (Ubangijinmu makusanci ne da mu mu yi asiri dashi, ko manisanci ne mukiraye shi?) to, hakika ni makusanci ne (dasu da sani na,) ina amsa rokon mai roko idan ya roke ni (in bashi abinda ya roka,) to, su nemi amsawatada da'a gare ni su gaskiya dani auwama kan bada gaskiya da nidan ha.

BA'ALIN HUKUNCE - HUKUNCE DA TAKE SAJE DA AZUMI)

أُحِلَّ لَكُمْ لَيْلَةَ الصِّيَامِ الرَّفَثُ إِلَىٰ نِسَآئِكُمْۚ هُنَّ لِبَاسٌ
لَّكُمْ وَأَنتُمْ لِبَاسٌ لَّهُنَّۗ عَلِمَ اللَّهُ أَنَّكُمْ كُنتُمْ تَخْتَانُونَ
أَنفُسَكُمْ فَتَابَ عَلَيْكُمْ وَعَفَا عَنكُمْۖ فَالْـَٰٔنَ بَاشِرُوهُنَّ
وَابْتَغُوا مَا كَتَبَ اللَّهُ لَكُمْۚ وَكُلُوا وَاشْرَبُوا حَتَّىٰ يَتَبَيَّنَ
لَكُمُ الْخَيْطُ الْأَبْيَضُ مِنَ الْخَيْطِ الْأَسْوَدِ مِنَ الْفَجْرِۖ
ثُمَّ أَتِمُّوا الصِّيَامَ إِلَى اللَّيْلِۚ وَلَا تُبَاشِرُوهُنَّ وَأَنتُمْ
عَٰكِفُونَ فِي الْمَسَٰجِدِۗ تِلْكَ حُدُودُ اللَّهِ فَلَا تَقْرَبُوهَاۗ
كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ اللَّهُ ءَايَٰتِهِۦ لِلنَّاسِ لَعَلَّهُمْ يَتَّقُونَ ﴿187﴾
وَلَا تَأْكُلُوا أَمْوَٰلَكُم بَيْنَكُم بِالْبَٰطِلِ وَتُدْلُوا بِهَا إِلَى
الْحُكَّامِ لِتَأْكُلُوا فَرِيقًا مِّنْ أَمْوَٰلِ النَّاسِ بِالْإِثْمِ
وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿188﴾ * يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ الْأَهِلَّةِۖ قُلْ هِيَ مَوَٰقِيتُ
لِلنَّاسِ وَالْحَجِّۗ وَلَيْسَ الْبِرُّ بِأَن تَأْتُوا الْبُيُوتَ مِن ظُهُورِهَا
وَلَٰكِنَّ الْبِرَّ مَنِ اتَّقَىٰۗ وَأْتُوا الْبُيُوتَ مِنْ أَبْوَٰبِهَاۚ وَاتَّقُوا اللَّهَ
لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿189﴾ وَقَٰتِلُوا فِي سَبِيلِ اللَّهِ الَّذِينَ
يُقَٰتِلُونَكُمْ وَلَا تَعْتَدُوٓاْۚ إِنَّ اللَّهَ لَا يُحِبُّ الْمُعْتَدِينَ ﴿190﴾

ربع

186. An halatta muku saduwa da matanku a cikin daran azumin (Ramalan), su tufafi ne gareku, ku tufafi ne garesu (watau ma-bukata junane ku) Allah yasan hak̃ik̃a ku kun kasance kuna ha'intar kawukanku, da jima'i a cikin daren azumin Ramalan (wannan ya afku ga Sayyadina Umaru da waninsa su kai hanzari ga Annabi Sallallahu alaihi wasallama) saboda haka Allah ya karɓi tubankuyi rangwami ga barinku. a yanzu (daya halatta muku wannan,) ku taradasu, ku nemi abinda Allah ya halatta a gareku (na daga saduwa dasu, saboda neman karuwa,) kuci kusha (a cikin dare dukkansa) har sai farin zare al-fijir ya bayyana a gareku daga bak̃in zare (buji-bujin dare,) sannan ku cika azumi (daga hudowan al-fijir) zuwa faɗuwar rana, kadaku, rungumi matayenku alhali ku kuna i'tikafi a masallaci, wadanean anka (hukunce hukunce ababan ambato) haddodin Allah ne (daya iyakancesu a gareku,) to, kadaku. kusance ta, tamfar yadda Allah ya bayyana muku abinda aka ambata yake bayyana ayoyinsa ga mutane, dan hak̃ik̃a su tsorace shi (kadasu saɓe shi).

(RASHAWA DA CIN HANCI)

187. Kada kuci dukiyoyinku tsakaninku, ta haramtacciyar hanya - (rashawa, sata, zamba) kadaku .kusanta ta zuwa mahukunta dan kuci yanki daga dukiyoyin mutane tareda zunubi alhali ku kun san (mabarnata ne ku).

(SASSABAWAR KAMANNIN WATADA SARA SABUWAR KOFA DAN RIYAWAR IBADA, KO DA'AWAR TA-SIRI)

188. Suna tambayarka (ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama) ga (hikimar) jirajiran wata (danme take bayyana sihiri, sannan ta cika da haske, sannan ta koma yandata bayyana, ba tana hali daya kamar rana ba?) Cene (dasu) "Ita lokatai ne ga mutane (da itane suke sanin k̃irgar makwanni da lokatan shuka da ciniki da idda da azumi da zakka da i'dodi) da (ita kuma suke sanin lokacin) Hajjinsu". Zuwar-wa ɗakuna ta bayanta ba nagarta ne ba, (suna sara sabuwar k̃ofa da zasu shigasu fita daga gare ta a lokacin harama da Hajji.) Kaidai wanda yaji tsoron Allah shine mai nagarta, kuzowa dakuna ta k̃ofofinta, (a cikin ih'rami da waninsa,) kuji tsoron Allah dan hak̃ik̃a kwa tsira.

(YAK̃I SABODA ALLAH DA LADA-BANSA)

189. Ku yak̃i wadanda suke yak̃arku (na kafirai) saboda inganta Addinin Allah, kada kuyi shishshigi (da fara yak̃insu,) Ubangiji bayason masu shishshigi (Mansuhiyace da ayar bara'atu).

وَاقْتُلُوهُمْ حَيْثُ ثَقِفْتُمُوهُمْ وَأَخْرِجُوهُم مِّنْ حَيْثُ أَخْرَجُوكُمْ
وَالْفِتْنَةُ أَشَدُّ مِنَ الْقَتْلِ وَلَا تُقَٰتِلُوهُمْ عِندَ الْمَسْجِدِ الْحَرَامِ حَتَّىٰ يُقَٰتِلُوكُمْ
فِيهِ فَإِن قَٰتَلُوكُمْ فَاقْتُلُوهُمْ كَذَٰلِكَ جَزَآءُ الْكَٰفِرِينَ ﴿190﴾ فَإِنِ
انتَهَوْاْ فَإِنَّ اللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿191﴾ وَقَٰتِلُوهُمْ حَتَّىٰ لَا تَكُونَ فِتْنَةٌ وَيَكُونَ
الدِّينُ لِلَّهِ فَإِنِ انتَهَوْاْ فَلَا عُدْوَٰنَ إِلَّا عَلَى الظَّٰلِمِينَ ﴿192﴾ الشَّهْرُ الْحَرَامُ
بِالشَّهْرِ الْحَرَامِ وَالْحُرُمَٰتُ قِصَاصٌ فَمَنِ اعْتَدَىٰ عَلَيْكُمْ فَاعْتَدُواْ عَلَيْهِ
بِمِثْلِ مَا اعْتَدَىٰ عَلَيْكُمْ وَاتَّقُواْ اللَّهَ وَاعْلَمُواْ أَنَّ اللَّهَ مَعَ الْمُتَّقِينَ ﴿193﴾
وَأَنفِقُواْ فِي سَبِيلِ اللَّهِ وَلَا تُلْقُواْ بِأَيْدِيكُمْ إِلَى التَّهْلُكَةِ وَأَحْسِنُواْ
إِنَّ اللَّهَ يُحِبُّ الْمُحْسِنِينَ ﴿194﴾ وَأَتِمُّواْ الْحَجَّ وَالْعُمْرَةَ لِلَّهِ فَإِنْ أُحْصِرْتُمْ
فَمَا اسْتَيْسَرَ مِنَ الْهَدْيِ وَلَا تَحْلِقُواْ رُءُوسَكُمْ حَتَّىٰ يَبْلُغَ الْهَدْيُ مَحِلَّهُ
فَمَن كَانَ مِنكُم مَّرِيضًا أَوْ بِهِ أَذًى مِّن رَّأْسِهِ فَفِدْيَةٌ مِّن صِيَامٍ
أَوْ صَدَقَةٍ أَوْ نُسُكٍ فَإِذَا أَمِنتُمْ فَمَن تَمَتَّعَ بِالْعُمْرَةِ إِلَى الْحَجِّ
فَمَا اسْتَيْسَرَ مِنَ الْهَدْيِ فَمَن لَّمْ يَجِدْ فَصِيَامُ ثَلَٰثَةِ أَيَّامٍ فِي الْحَجِّ وَسَبْعَةٍ
إِذَا رَجَعْتُمْ تِلْكَ عَشَرَةٌ كَامِلَةٌ ذَٰلِكَ لِمَن لَّمْ يَكُنْ أَهْلُهُ حَاضِرِي
الْمَسْجِدِ الْحَرَامِ وَاتَّقُواْ اللَّهَ وَاعْلَمُواْ أَنَّ اللَّهَ شَدِيدُ الْعِقَابِ ﴿195﴾

190. Ku yaƙe su inda duk kuka samesu kufid dasu ta inda suka fid daku (Makka, an kwayi musu haka din shekarar bude Makka,) mushirikancinsu yafi kisansu (a cikin harami da ihra'mi wanda suka ga girmansa,) kadaku ,yaƙesu nan ga masallaci mai alfarma sai sun yakeku a cikinsa, in sun yakeku (a cikinsa) ku yaƙesu (a cikinsa,) sakamakon kafirai kamar wancananka (kisa da fitarwa) yake.

191. In suka hanu (ga barin kafirci suka Musulunta,) to, haƙiƙa Ubangiji mai yawan gafara ne (garesu) mai yawan jinƙai.

192. Ku yaƙesu har kada a samu shirka, Addini yazamo ga Allah (Shi kaɗai,) in suka hanu (ga barin shirka) to, (kada kiyi shishshigi a kansu) bashishshigi (da kisa ko waninsa) sai bisa azzalimai.

193. Wata mai alfarma daidai yakeda wata mai alfarma, alfarmatai abin yiwa sakayyace, saboda haka duk wanda yayi shishshigi a kanku dayaƙi (cikin harami ko ihrami ko waninsu,) kuyi shishshigi a kansa da irin shishshigin da sukai a kanku, kuji tsoron Allah (a cikin shishshigi da waninsa,) ku sani haƙiƙa Allah yana tareda masu tsoronsa, (da nasara da taimako).

194. Kuciyar a cikin inganta Addinin Allah (yaƙi ko waninsa,) kada kuyi jifa da kawukanku zuwa halaka, (da ƙin ciyarwa a cikin yaƙi ko barin yaƙin ko wani abu mai kamar haka,) ku kyautata (a cikin ciyarwa da waninta,) haƙiƙa Allah yana son masu kyautatawa.

(HAJJI DA SASHEN HUKUNCE-HU-KUNCENSA)

195. Kuyi cikakken Hajji da cikakkiyar Umra dan Allah, idan aka tsareku (ga barin cikasu da magauci,) to, abinda ya sawwaƙa na hadaya (yana kanku, akuya,) kadaku ,aske kawunanku dan warware hajji sai hadaya ta kai warinta (shine gurin tsarewa nan ga Shafi'i da Maliki) to, duka wanda ya kasance marar lafiya daga cikinku, ko akwai cutuwa gareshi daga kansa, (kamar kwarkwata ko ciwon kai, yayi aski cikin ihrami) to, fidiya (na kansa) ta azumin (kwana uku,) ko sadakar kwanan sha uku, na daga marinjayin abincin gari) ko ta akuya, to, idan kun amince (magauci, shine ya tafi ko yazam badu shi) to, wanda yaji daɗi da Umra (saboda yagamata yayi wani abu daga abin haramtawar ihrami) zuwa harama da hajji, to, abinda ya sawwaƙa na hadaya (na kansa,) wanda bai sami hadaya ba, azumin kwana uku (na kansa) a cikin halin harama da hajji da kwana bakwai idan kuka koma zuwa mazauninku, Makka ko waninta, wancananka gomace cikakkiya, wannan (hukunci) na wanda iyalinsa basu kasance mazauna masallaci mai alfarma ne ba, (shine basu kasance a bisa koma baya daga zango biyu badaga harami nan ga Shafi'i da Maliki). Kuji tsoron Allah, ku sani haƙiƙa Allah mai tsanain uƙubane (ga wanda ya saɓa masa).

ثمن

۞ الْحَجُّ أَشْهُرٌ مَّعْلُومَاتٌ فَمَن فَرَضَ فِيهِنَّ الْحَجَّ
فَلَا رَفَثَ وَلَا فُسُوقَ وَلَا جِدَالَ فِي الْحَجِّ وَمَا تَفْعَلُوا
مِنْ خَيْرٍ يَعْلَمْهُ اللَّهُ وَتَزَوَّدُوا فَإِنَّ خَيْرَ الزَّادِ
التَّقْوَىٰ وَاتَّقُونِ يَا أُولِي الْأَلْبَابِ لَيْسَ عَلَيْكُمْ
جُنَاحٌ أَن تَبْتَغُوا فَضْلًا مِّن رَّبِّكُمْ فَإِذَا أَفَضْتُم
مِّنْ عَرَفَاتٍ فَاذْكُرُوا اللَّهَ عِندَ الْمَشْعَرِ الْحَرَامِ
وَاذْكُرُوهُ كَمَا هَدَاكُمْ وَإِن كُنتُم مِّن قَبْلِهِ
لَمِنَ الضَّالِّينَ ﴿196﴾ ثُمَّ أَفِيضُوا مِنْ حَيْثُ أَفَاضَ النَّاسُ
وَاسْتَغْفِرُوا اللَّهَ إِنَّ اللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿197﴾ فَإِذَا
قَضَيْتُم مَّنَاسِكَكُمْ فَاذْكُرُوا اللَّهَ كَذِكْرِكُمْ
ءَابَاءَكُمْ أَوْ أَشَدَّ ذِكْرًا فَمِنَ النَّاسِ مَن يَقُولُ
رَبَّنَا ءَاتِنَا فِي الدُّنْيَا وَمَا لَهُ فِي الْآخِرَةِ مِنْ خَلَاقٍ ﴿198﴾
وَمِنْهُم مَّن يَقُولُ رَبَّنَا ءَاتِنَا فِي الدُّنْيَا حَسَنَةً
وَفِي الْآخِرَةِ حَسَنَةً وَقِنَا عَذَابَ النَّارِ ﴿199﴾ أُولَٰئِكَ
لَهُمْ نَصِيبٌ مِّمَّا كَسَبُوا وَاللَّهُ سَرِيعُ الْحِسَابِ ﴿200﴾

196. Hajji watannine ababan sani (Shawwal, Zilƙida da kwana goma na Zil-hijja,) to, wanda ya wajabta haji a cikinsu (a kansa,) to, babu batsa, (a cikinsa,) ba fasiƙanci, ba husuma a cikin hajji, duk abinda kuka aikata na alhairi Allah yasanshi, kuyi (ishashshan) guzuru haƙiƙa fiyayyen guzuri abindazai hanaka rance (wurin wani, ko roƙonsa,) kuji tsorona ya ma'abota hankula.

(BA'ALIN HUKUNCE-HUKUNCEN HAJJI)

197. Babu laifi a kanku (a cikin) ku nemi arziki daga Ubangijinku (da ciniki a hajji,) idan kuka iso daga Arfa (bayan kun gama tsayuwa,) to, ku ambaci Allah (bayan kwana a Muzdalifa da Talbiyya, da Hailala, da Addu'a) nan ga Mash'aril-Harami (dutsene a ƙarshen Muzdalifa anace masa kuzahu, wanda Annabi Sallallahu alaihi wasallama ya tsaya nan gareshi yana roƙon Allah har haske ya faifaye ƙwarai,) ku ambace shi dan yasanar daku alamomin Addininku, haƙiƙa kun kasance gaban shiryarwar Ubangiji daga cikin ɓatattu.

198. Sannan ku izo (yaku kuraishawa) ta inda mutane suke izowa (ai daga Arfa, ku tsaya a Arfa taredasu, maimakon tsayuwarku a Musdalifa dan jin girma,) ku nemi gafarar Allah (daga zunibanku) Ubangiji mai yawan gafara ne (ga mumimai) mai yawan jinƙai (dasu).

199. To, idan kuka gama ibadodin hajjinku (da jifan jamratil -aƙabati, da ɗawafin ifa'la kuka komo Mina) to, ku ambaci Allah (da kabarbari da kirari,) kamar ambatanku, iyayanku (da kuke yi da in kum gama hajjinku saboda fariya,) ko fiye da ambaton iyayenku, to, akwai daga mutane wanda yake cewa "Ya Ubangijinmu! bamu nasibinmu (1) a duniya, "to, (a bashi a cikinta) a lahira ko, bashi da Nasibi (ko kaɗan) akwai daga cikinsu wanda yake cewa "Ya Ubangijinmu! bamu ni'ima a duniya, bamu Aljanna a Lahira, kiyashe mu azabar wuta".

200. Waɗancananka suna da sakamako dan abinda suka aikata (na hajji da addu'a da waninsa,) Allah mai garajen sakamako ne, (zai yiwa halitta dukkansu sakamako a gwargwadon rabin wuni daga kwanikan duniya, saboda hadisin daya faɗi haka).

حزب

* وَاذْكُرُواْ اُ۬للَّهَ فِےٓ أَيَّامٖ مَّعْدُودَٰتٖۖ فَمَن تَعَجَّلَ فِے يَوْمَيْنِ
فَلَآ إِثْمَ عَلَيْهِۖ وَمَن تَأَخَّرَ فَلَآ إِثْمَ عَلَيْهِۖ لِمَنِ اِ۪تَّقَيٰۖ
وَاتَّقُواْ اُ۬للَّهَ وَاعْلَمُوٓاْ أَنَّكُمُۥٓ إِلَيْهِ تُحْشَرُونَۖ ﴿201﴾ وَمِنَ اَ۬لنَّاسِ
مَن يُعْجِبُكَ قَوْلُهُۥ فِے اِ۬لْحَيَوٰةِ اِ۬لدُّنْيا وَيُشْهِدُ اُ۬للَّهَ عَلَيٰ مَا فِے قَلْبِهِۦ
وَهُوَ أَلَدُّ اُ۬لْخِصَامِۖ ﴿202﴾ وَإِذَا تَوَلَّيٰ سَعَيٰ فِے اِ۬لْأَرْضِ لِيُفْسِدَ
فِيهَا وَيُهْلِكَ اَ۬لْحَرْثَ وَالنَّسْلَۖ وَاللَّهُ لَا يُحِبُّ اُ۬لْفَسَادَۖ ﴿203﴾
وَإِذَا قِيلَ لَهُ اُ۪تَّقِ اِ۬للَّهَ أَخَذَتْهُ اُ۬لْعِزَّةُ بِالْإِثْمِۖ فَحَسْبُهُۥ
جَهَنَّمُۖ وَلَبِئْسَ اَ۬لْمِهَادُۖ ﴿204﴾ وَمِنَ اَ۬لنَّاسِ مَن يَّشْرِے
نَفْسَهُ اُ۪بْتِغَآءَ مَرْضَاتِ اِ۬للَّهِۖ وَاللَّهُ رَءُوفُۢ بِالْعِبَادِۖ ﴿205﴾
يَٰٓأَيُّهَا اَ۬لذِينَ ءَامَنُواْ اُ۟دْخُلُواْ فِے اِ۬لسِّلْمِ كَآفَّةٗۖ
وَلَا تَتَّبِعُواْ خُطُوَٰتِ اِ۬لشَّيْطَٰنِۖ إِنَّهُۥ لَكُمْ عَدُوّٞ
مُّبِينٞۖ ﴿206﴾ فَإِن زَلَلْتُم مِّنۢ بَعْدِ مَا جَآءَتْكُمُ
اُ۬لْبَيِّنَٰتُ فَاعْلَمُوٓاْ أَنَّ اَ۬للَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌۖ ﴿207﴾
هَلْ يَنظُرُونَ إِلَّآ أَن يَأْتِيَهُمُ اُ۬للَّهُ فِے ظُلَلٖ مِّنَ اَ۬لْغَمَامِ
وَالْمَلَٰٓئِكَةُ وَقُضِيَ اَ۬لْأَمْرُۖ وَإِلَى اَ۬للَّهِ تَرْجِعُ اُ۬لْأُمُورُۖ ﴿208﴾

201. Ku ambaci Ubangiji (da kabarbari yayin jifan Jamaratu) a cikin kwanika ababan ƙirgawa, (kwanikan yanyane guda uku,) to, wanda yayi gaggawa (da izowa daga Mina) a cikin kwana biyu, (a cikin rana ta biyu daga kwanikan yanyane bayan jifan tsakwan-kwaninsa) babu laifi a gareshi, wanda yayi jinkiri (a Mina ya kwana a daren uku, ya jefa tsakwan-kwaninsa) babu laifi a gareshi (rashin laifin nan ya tabbata) ga wanda yaji tsoron Allah, (domin shine Alhaji a haƙiƙa (duk wanda yayi hajji baiji tsoron Allah a cikin aikin hajjin ba, to, ba hajji yayi ba, hajijiya yayi). kuji tsoron Allah a kowane hali, hajji ko wa-ninsa) ku sani haƙiƙa ku ana taraku zuwa gareshi.

(WANI ABU DAGA ALAMOMIN NIFAƘI HAR YAU)

202. Akwai daga mutane wanda maganarsa take ƙayatar dakai a rayuwar duniya, (bazata ƙayatar dakai a Lahira ba, saboda saɓawarsa abinda yake kudurinsa,) yake shaidad da Allah a kan abinda yake cikin zuciyarsa, (cewa shimai dacewa ne da maganarsa,) alhali shimai tsananin husuma ne (gareka, da maƙiyanka saboda adawarsa gareka, shine Akhnas dan Shariku, munafiki ne mai zaƙin harshe ga Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) wannan aya ta kama dukan wanda yayi aiki irin nasa).
203. Idan ya juya (ga barinka) saiya tafi a cikin ƙasa, dan yayi ɓarna a cikinta, ya halakad da shuka da zirriya, Allah bayason ɓarna.
204. Idan ance dashi: "Ji tsoron Allah (cikin aikin ka,)" sai homa ta kama shi (watau, takabburanci a kan mummunan aiki,) jahannama ta isheshi, Lallai tir! dashimfida (ita).
205. Akwai daga mutane wanda yake bada ransa a cikin neman yardar Allah, (shine Suhaibu Arrumi da irinsa, mushirikai sun dame shi da cuta , ya ƙaura zuwa Madina, yabar musu dukiyarsa.) Allah mai tsananin jinƙai ne ga bayi.

(WANDA BAI BI DUKKAN HUKUNCE-HUKUNCEN ADDINI BADA SAKAMAKONSA)

206. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! ku shiga cikin Musulunci baki ɗaya, (a cikin dukkan hukunce-hukuncensa,) kada kubi ƙawace-ƙawacen shaiɗan, haƙiƙa shi magauci ne a gareku mabayyanin ƙiyayya.
207-Idan kuka karkata (ga barin shiga a cikin dukkan hukunce-hu-kuncensa,) bayan hujjoji mabayyana sunzo muku (a kan cewa shi gaskiya ne) to, kusani haƙiƙa Allah mabuwayi ne gwanine (a cikin aikinsa).
208. (Masu karkacewar nan) basa saurаron komi sai (azabar)Allah tazo musu daga rumfuna na girgije, da Mala'iku, angama da Lamarinsu, zuwa Allah al'amura suke komawa.

1) Rabonnu ko sakamakonmu.

سَلْ بَنِيٓ إِسْرَآءِيلَ كَمْ ءَاتَيْنَٰهُم مِّنْ ءَايَةٍ بَيِّنَةٍ وَمَنْ يُّبَدِّلْ نِعْمَةَ
اَ۬للَّهِ مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَتْهُ فَإِنَّ اَ۬للَّهَ شَدِيدُ اُ۬لْعِقَابِ ﴿209﴾ زُيِّنَ
لِلَّذِينَ كَفَرُواْ اُ۬لْحَيَوٰةُ اُ۬لدُّنْيَا وَيَسْخَرُونَ مِنَ اَ۬لَّذِينَ ءَامَنُواْ
وَالَّذِينَ اَ۪تَّقَوْاْ فَوْقَهُمْ يَوْمَ اَ۬لْقِيَٰمَةِ وَاللَّهُ يَرْزُقُ مَنْ يَّشَآءُ بِغَيْرِ حِسَابٍ ﴿210﴾
* كَانَ اَ۬لنَّاسُ أُمَّةً وَٰحِدَةً فَبَعَثَ اَ۬للَّهُ اُ۬لنَّبِيٓـِٔينَ مُبَشِّرِينَ
وَمُنذِرِينَ وَأَنزَلَ مَعَهُمُ اُ۬لْكِتَٰبَ بِالْحَقِّ لِيَحْكُمَ بَيْنَ اَ۬لنَّاسِ فِيمَا
اَ۪خْتَلَفُواْ فِيهِ وَمَا اَ۪خْتَلَفَ فِيهِ إِلَّا اَ۬لَّذِينَ أُوتُوهُ مِنۢ بَعْدِ
مَا جَآءَتْهُمُ اُ۬لْبَيِّنَٰتُ بَغْياَۢ بَيْنَهُمْ فَهَدَى اَ۬للَّهُ اُ۬لَّذِينَ ءَامَنُواْ
لِمَا اَ۪خْتَلَفُواْ فِيهِ مِنَ اَ۬لْحَقِّ بِإِذْنِهِۦ وَاللَّهُ يَهْدِے مَنْ يَّشَآءُ إِلَىٰ
صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿211﴾ أَمْ حَسِبْتُمُۥٓ أَن تَدْخُلُواْ اُ۬لْجَنَّةَ وَلَمَّا يَأْتِكُم
مَّثَلُ اُ۬لَّذِينَ خَلَوْاْ مِن قَبْلِكُم مَّسَّتْهُمُ اُ۬لْبَأْسَآءُ وَالضَّرَّآءُ
وَزُلْزِلُواْ حَتَّىٰ يَقُولُ اُ۬لرَّسُولُ وَالَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ مَتَىٰ نَصْرُ اُ۬للَّهِ أَلَآ إِنَّ
نَصْرَ اَ۬للَّهِ قَرِيبٌ ﴿212﴾ يَسْـَٔلُونَكَ مَاذَا يُنفِقُونَ قُلْ مَآ أَنفَقْتُم
مِّنْ خَيْرٍ فَلِلْوَٰلِدَيْنِ وَالْأَقْرَبِينَ وَالْيَتَٰمَىٰ وَالْمَسَٰكِينِ
وَابْنِ اِ۬لسَّبِيلِ وَمَا تَفْعَلُواْ مِنْ خَيْرٍ فَإِنَّ اَ۬للَّهَ بِهِۦ عَلِيمٌ ﴿213﴾

ثمن

209. (Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama!) tambayi Bani'israi'ila (dan urustawa dasu,) nawane muka basu na daga aya mabayyaniya (suka bitilce da ita) duk wanda ya bitilce ni'imar Allah bayan tazo masa, to, haƙiƙa Allah mai tsananin azabane (a gareshi).

210. An ƙawata rayuwar duniyaga wađanda suka kafirta (mutanen Makka da wađansunsu saboda haka suka, zuru a cikin son ta,) su suna izgili da wađanda suka bada gaskiya, (kamar Bilalu da Ammaru, dasuhaibu da masu kwaikwayonsu a yau,) wađanda suka tsoraci Allah (sune wađannan mutane) suna sama dasu ra-nar Al-ƙiyama, Allah yana azurta wanda yaga dama (dayalwataccen arzikin da) bazai kirgu ba (a duniya da lahira).

(BUƘATA IZUWA MANZANNI ALAI HIMUSSALAMU)

211. Mutane sun kasance al'umma guda đaya (a kan imani, suk sassaɓa, wađansu suka bada gaskiya wađansu suka kafirta, Allah ya aiko Annabawa (izuw garesu,) masu albishir (da aljanna ga wanda yabada gaskiya masu ban tsoro (da wuta, ga wanda ya kafirta,) ya saukar da littattafai taredasu da gaskiy don yayi hukunci dashi tsakanin mutane cikin abindasuk sassaɓa a cikinsa (na addini,) ba wanda yasaɓa a cikin addini nan sai wađanda aka basu Littattafai bayan zuwan hujjoji ma bayyana (a garesu a kan Tauhidi) don zalunci (na daga kafira;nan) a tsakaninsu, to, sai Allah ya shiryi wađanda suka bada gaskiyaga abinda suka sassaɓa a cikinsa na gaskiya da nufinsa Allah na shiriyar wanda yaga damar shiriyarsa izuwa tafarki madaidaici.

(ABINDA MANZANNI DA MUMINAI SUKE GAMUWA DASHI A CIKII HANYARSU TA KIRA IZUWA ALLAH)

212. Bari! Yalla kuna zaton kwa shiga Aljanna irin abinda ya sami wađanda suke gabanku (na muminai) bai same ku ba? Tsanin talauci yasamesu da rashin Lafiya, aka girgizasu (da dan gogin bala'i) har manzoda wadanda suka bada gaskiya taredashi suna cewa "Yaushe taimakon Allah?" (sai Allah amsa,) "Na'am! Haƙiƙa taimakon Allah makusanci ne".

(CIYARWA DA WANDA YAFI CANCANTADA ITA)

213. Suna tambayarka (Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama) me zasu ciyar, (Amru dan Jamuhune ya tambayi Annabi Sallallahu alaihi wasallama, shi tsohone mai dukiya gwargwadonme zai ciyar, su wazai ciyar?) Cene (dasu): " Abinda kuka ciyar na alhairi (komi ƙanƙantarsa,da yawansa,) to, ya tabbata ga mahaifa da makusanta, da marayu, da miskinai, da đan tafarki, duk abinda kuka aikata na alhairi (ciyarwa ko waninsa, to, haƙiƙa Allah masanine dashi".

(WANI ABU NA SHA'ANIN YAƘI A CIKIN MUSULUNCI)

كُتِبَ عَلَيْكُمُ الْقِتَالُ وَهُوَ كُرْهٌ لَّكُمْ وَعَسَىٰ أَن تَكْرَهُوا شَيْـًٔا
وَهُوَ خَيْرٌ لَّكُمْ وَعَسَىٰ أَن تُحِبُّوا شَيْـًٔا وَهُوَ شَرٌّ لَّكُمْ وَاللَّهُ يَعْلَمُ
وَأَنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴿214﴾ يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ الشَّهْرِ الْحَرَامِ
قِتَالٍ فِيهِ قُلْ قِتَالٌ فِيهِ كَبِيرٌ وَصَدٌّ عَن سَبِيلِ اللَّهِ
وَكُفْرٌ بِهِ وَالْمَسْجِدِ الْحَرَامِ وَإِخْرَاجُ أَهْلِهِ مِنْهُ أَكْبَرُ
عِندَ اللَّهِ وَالْفِتْنَةُ أَكْبَرُ مِنَ الْقَتْلِ وَلَا يَزَالُونَ يُقَاتِلُونَكُمْ
حَتَّىٰ يَرُدُّوكُمْ عَن دِينِكُمْ إِنِ اسْتَطَاعُوا وَمَن يَرْتَدِدْ
مِنكُمْ عَن دِينِهِ فَيَمُتْ وَهُوَ كَافِرٌ فَأُولَٰٓئِكَ حَبِطَتْ
أَعْمَالُهُمْ فِي الدُّنْيَا وَالْآخِرَةِ وَأُولَٰٓئِكَ أَصْحَابُ النَّارِ
هُمْ فِيهَا خَالِدُونَ ﴿215﴾ إِنَّ الَّذِينَ ءَامَنُوا وَالَّذِينَ هَاجَرُوا
وَجَاهَدُوا فِي سَبِيلِ اللَّهِ أُولَٰٓئِكَ يَرْجُونَ رَحْمَتَ اللَّهِ
وَاللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿216﴾ * يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ الْخَمْرِ وَالْمَيْسِرِ ربع
قُلْ فِيهِمَا إِثْمٌ كَبِيرٌ وَمَنَافِعُ لِلنَّاسِ وَإِثْمُهُمَا أَكْبَرُ
مِن نَّفْعِهِمَا وَيَسْـَٔلُونَكَ مَاذَا يُنفِقُونَ ﴿217﴾ قُلِ الْعَفْوَ
كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ اللَّهُ لَكُمُ الْآيَاتِ لَعَلَّكُمْ تَتَفَكَّرُونَ فِي الدُّنْيَا وَالْآخِرَةِ

214. An wajabta muku yaƙin kafirai, alhali shi abin ƙine a gurin ku (Dan-Adam bayason wahala) Yakusanta, kuƙi abu alhali, shine alhairi a gareku, Yakusanta ku so abu alhali sharri ne a gareku, (saboda dan Adam mai biyewa sha'awa ne) Allah yasan (abinda yafi a gareku,) ku baku san (wanda yafi ba, sai kuyi gaggawa izuwa abinda ya umarce ku dashi).

215. Suna tambayar ka ga wata mai alfarma yaƙi a cikinsa, cene da (dasu) "yaƙi a cikinsa maigirman zunubi ne, hana mutane ga barin addinin Allah, da kafircewa da Allah da hana masallaci mai alfarma Makka, da fitar da mutanensa daga cikinsa (Annabi Sallallahu alaihi wasallama da muminai) shiyafi girman zunubi nan ga Allah, (daga yaƙi cikin wata mai alfarma)" Mushirikancinku yafi girma daga kasheku (a cikinsa,) kafirai bazasu gushebasuna yaƙarku (ku muminai) donsu juyar daku ga barin addininku (izuwa kafirci) in sun sami iko, duk wanda yayi ridda daga cikinku ga barin addininsa, to, ya mutu alhali yana kafiri, to, waɗancananka ayyukansu (na gari) sun lalace a duniya da lahira, waɗancananka sune 'yan wuta, su madauwama ne a cikinta.

216. Waɗanda suka bada gaskiya da waɗanda sukayi hijira, sukayi jihadi a cikin inganta addinin Allah, waɗancananka suna ƙaunar rahamar Allah, Ubangiji mai yawan gafara ne (ga muminai) mai yawan jinƙai (dasu).

(GIYA DA CACA DA HUKUNCINSU)

217. Suna tambayarka ga giya da caca (Meye hunkuncinsu?) Cene (dasu) "Akwai zunubi mai girma a cikin yinsu, (saboda abinda yake faruwa daga garesu na daga husuma, da zage-zage, da alfasha,) da amfani ga masuyi, (jin daɗi da farin ciki a cikin giya da samun dukiya bada wahala ba, a cikin caca,) ɓarnace-barnacen dake cikinsu, yafi amfanin da yake cikinsu" (yayin da wannan aya ta sauka waɗansu mutane suka shata waɗansu kuma suka hanu, saida ayar Ma'ida tazo dayankakken hani).

(WANI ABU DAGA MAGANAR CIYARWA HAR YAU)

Suna tambayarka meye. gwargwadon abinda zasu ciyar? Cene, "Su ciyar da abinda ya kinginta ga barin bukatarsu, (watau abinda bukatarsu bata shafe shi ba)" tamfar da Allah yayi muku bayanin abinda aka ambata yake muku bayanin ayoyi, don haƙiƙa kuyi tunani a cikin al'amarin duniya da lahira (ku riƙi abinda yafi amfani a gareku a cikinsu).

(WALITTA A KAN DUKIYAR MARAYA)

وَيَسْـَٔلُونَكَ عَنِ الْيَتَٰمَىٰ قُلْ إِصْلَاحٌ لَّهُمْ خَيْرٌ
وَإِن تُخَالِطُوهُمْ فَإِخْوَانُكُمْ وَاللَّهُ يَعْلَمُ الْمُفْسِدَ مِنَ الْمُصْلِحِ
وَلَوْ شَآءَ اللَّهُ لَأَعْنَتَكُمْ إِنَّ اللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿218﴾
وَلَا تَنكِحُوا الْمُشْرِكَاتِ حَتَّىٰ يُؤْمِنَّ وَلَأَمَةٌ مُّؤْمِنَةٌ خَيْرٌ مِّن مُّشْرِكَةٍ
وَلَوْ أَعْجَبَتْكُمْ وَلَا تُنكِحُوا الْمُشْرِكِينَ حَتَّىٰ يُؤْمِنُوا وَلَعَبْدٌ مُّؤْمِنٌ
خَيْرٌ مِّن مُّشْرِكٍ وَلَوْ أَعْجَبَكُمْ أُولَٰٓئِكَ يَدْعُونَ إِلَى النَّارِ
وَاللَّهُ يَدْعُوا إِلَى الْجَنَّةِ وَالْمَغْفِرَةِ بِإِذْنِهِ وَيُبَيِّنُ ءَايَاتِهِ
لِلنَّاسِ لَعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿219﴾ وَيَسْـَٔلُونَكَ عَنِ الْمَحِيضِ
قُلْ هُوَ أَذًى فَاعْتَزِلُوا النِّسَآءَ فِي الْمَحِيضِ وَلَا تَقْرَبُوهُنَّ
حَتَّىٰ يَطْهُرْنَ فَإِذَا تَطَهَّرْنَ فَأْتُوهُنَّ مِنْ حَيْثُ أَمَرَكُمُ اللَّهُ
إِنَّ اللَّهَ يُحِبُّ التَّوَّابِينَ وَيُحِبُّ الْمُتَطَهِّرِينَ ﴿220﴾ نِسَآؤُكُمْ
حَرْثٌ لَّكُمْ فَأْتُوا حَرْثَكُمْ أَنَّىٰ شِئْتُمْ وَقَدِّمُوا لِأَنفُسِكُمْ
وَاتَّقُوا اللَّهَ وَاعْلَمُوا أَنَّكُم مُّلَاقُوهُ وَبَشِّرِ الْمُؤْمِنِينَ ﴿221﴾
وَلَا تَجْعَلُوا اللَّهَ عُرْضَةً لِّأَيْمَانِكُمْ أَن تَبَرُّوا
وَتَتَّقُوا وَتُصْلِحُوا بَيْنَ النَّاسِ وَاللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿222﴾

218. Suna tambayarka ga sha'anin marayu (in sunci dukiyarsu sunyi laifi? Idan suka ware dukiyarsu ga barin tasu suka basu abincinsu, sun ƙwaru?) Cene (dasu) "Gyara musu dukiyarsu ta fuskar cuɗe-ne in-cuɗe-ka, yin muhaɗa dasu (watau kuka shigar da kuɗinku a cikin kuɗinsu to, 'yan'uwankune (a cikin addini, watau yin wannan halal ne a gareku don shine zumunci,) Allah yasan mai ɓarna (ga dukiyoyinsu) daga mai gyara, da Allah yaga dama dayaƙuntata a gareku (da haramcin cuɗanye,) haƙiƙa Ubangiji marinjayi ne (cikin al'amarinsa) gwani (cikin aikinsa)".

(HARAMCIN AUREN MUSULMI BADA MUSULMA BA)

219. (Ku Musulmi) kadaku ,auri mataye kafirai sai sun bada gaskiya, haƙiƙa kuyanga Musulma ita tafi daga'ya kafira, kodata ƙayatar daku (da kyantada dukiyarta sai ko in Bakitaɓa ce,) kadaku aurawa kafirai mataye Musulmai sai sun Musulunta, haƙiƙa bawa Musulmi shi yafi daga kafiri, kodaya ƙayatar daku ,(da dukiyarsa da kyansa) waɗancananka kafirai suna kira izuwa wuta ne (bai kamata a aure su ba). Allah yana kira izuwa Aljanna ne da gafara (da harshen manzanninsa) da sanyewarsa(da izininsa da nufinsa) (saboda haka ya wajaba a amsa masa da aurawa Masowansa -watau musulmi yana bayyana ayoyinsa ga mutane don haƙiƙa su, su wa'azantu.

HAILA DA HUKUNCINTADA SADUWA DA MATADA LADABINSA)

220. Suna tambayar ka ga haila, (yaya mata zasuyi a cikinta?) Cene (dasu) "Ita haila ƙazantace, ku janyewa mataye a cikin haila kadaku ,kusance su (da jima'i) sai sunyi wanka (bayan yankewarsa,) idan sukayi wanka, to, kuzo musu (da jima'i) ta inda Allah ya umarce ku, (watau ta gaba bata baya ba,) haƙiƙa Allah yana son masu yawan tuba (daga zunubi) yana son masu tsarkaka (daga dukkan ƙazanta).

221. Matayenku gonar (shuka 'ya'ya) ce a gareku, ku zowa gonarku, (ai farjin matayenku). yadda kuka ga dama, (shine a tsaye ko a zaune, ko a kishingiɗe, ko reras, ko a kife) ku gabatar da aiki kyakkyawa ga kanku, (ambaton Bisimilla da neman tsari daga sharrin Shaiɗan da niyyar yawaita al'ummar Annabi Sallallahu alaihi wasallama). Ku tsoraci Ubangiji (a cikin umarninsa da hane-hanensa,) ku sani haƙiƙa ku zaku haɗu dashine (a tashin al-ƙiyama) don yiwa muminan (da suka tsorace shi) albishir (da aljanna).

(RANTSUWA DA ALLAH)

222. Kadaku ,sanya Allah tomo (watau karewa ga kubi Allah ku tsorace shi) saboda rantse-rantsenku a kan bazakuyi aikin alhairi da tsoron Allah ba, (wanda ya rantse da haka kuwa ya karya rantsuwar sai yayi kaffara, wanda kuma ya rantse a kan zaiyi ɗa' a, to wannan rantsuwar ɗa'a ce) kuma kadaku maida rantsuwa dasunan Allah tomo a kan bazakuyi gyara tsakanin mutane ba, Allah mai jin (magan-ganunkune da haluluwanku,) masanine (da maganganunkuda haluluwanku).

لا يؤاخذكم الله باللغو في أيمانكم ولكن يؤاخذكم بما كسبت
قلوبكم والله غفور حليم 223 للذين يؤلون من نسائهم تربص
أربعة أشهر فإن فاءو فإن الله غفور رحيم 224 وإن عزموا
الطلاق فإن الله سميع عليم 225 * والمطلقات يتربصن بأنفسهن
ثلاثة قروء ولا يحل لهن أن يكتمن ما خلق الله في أرحامهن
إن كن يؤمن بالله واليوم الآخر وبعولتهن أحق بردهن في ذلك
إن أرادوا إصلاحا ولهن مثل الذي عليهن بالمعروف وللرجال
عليهن درجة والله عزيز حكيم 226 الطلاق مرتان فإمساك
بمعروف أو تسريح بإحسان ولا يحل لكم أن تأخذوا مما آتيتموهن
شيئا إلا أن يخافا ألا يقيما حدود الله فإن خفتم ألا يقيما
حدود الله فلا جناح عليهما فيما افتدت به تلك حدود الله فلا تعتدوها
ومن يتعد حدود الله فأولئك هم الظالمون 227
فإن طلقها فلا تحل له من بعد حتى تنكح زوجا غيره
فإن طلقها فلا جناح عليهما أن يتراجعا إن ظنا أن يقيما
حدود الله وتلك حدود الله يبينها لقوم يعلمون 228

223. Allah baya kamakuda rantsuwa yashashshiya wacce take gudana kan harshe bada niyya ba, (ba laifi a cikinta bakaffara) sai dai yana riƙon kune da abinda zukatanku suka tsuwurwurta, (ai kuka nufa a zuciyarku na rantsuwa, idan kun ƙarya,) Ubangiji mai yawan gafara ne (ga ya-shashshiyar rantsuwa da waninta) mai jinkirin azabane (ga wanda ya cancanceta).

(ILA'I - WATAU KIN KUSATAR MACE SABODA RANTSUWA)

224. Sauraron wata hudu ya tabbata ga waɗannan da sukayi rantsuwa daga matayensu, (ai suka rantse bazasu kusace su ba wata huɗu,) idan suka komo daga rantsuwa (izuwa wada'i a cikin waɗannan watanni ko bayansu) to, haƙiƙa Allah mai gafara ne (a garesu ga cutar da suka yiwa matansu da rantsuwa) mai jinƙai (dasu).

225. In ko sukayi niyyar shika, (basu komo ba, to, su aukar dashikan) to, haƙiƙa Ubangiji mai jine (ga maganarsu da niyarsu,) masanine (da maganarsu da niyarsu, ai baza a sake sauraronsu ba, bayan cikar wata huɗu, saisu komo ko su shika).

(KUBUTAR MAHAIFA A CIKIN SHIKA DA BA'ALIN HUKUNCE-HUKUNCENSA)

226. Mataye ababan shika (waɗanda akayi duhuli dasu) su saurari tsarki ukuda kawukansu, bai halatta garesu, su ɓoye abinda Allah ya halitta a cikin mahaifarsu ba, (na daga da koko laifuka) in sun kasance sun bada gaskiya da Allah da ranar Lahira, mazajensu sune sukafi cancantada mayar dasu a cikin zamanin sauraron nan in sun nufi gyara tsakaninsu (ba cutar da mace ba).

(MATADA HAƘƘOƘINSU A CIKIN AURE)

Su mataye suna da haƙƙi a kan maza irin wanda maza suke dashi a kansu da abin sani (a shari'a na daga kyan zama da barin cutarwa,) maza suna da daraja a kan mata (a cikin haƙƙi na wajabcin ɗa'a garesu, saboda sadaki da ciyarwa) Allah mabuwayi ne (a cikin mulki) gwanine (a cikin abinda ya shirya a cikin halittarsa).

(BA'ALIN HUKUNCE-HUKUNCEN SHIKA)

227. Shika marra biyu ne, ku riƙesu da abin sani (a shari'a) ko saki da kyautatawa, bai halatta gareku (yaku mazaje) ku riƙi wani abu daga abinda kuka basu (na daga sadaki) ba, sai ko in ma'auran guda biyu sunji tsoron bazasu tsaida haddodin Allah ba, to, idan kunji tsoron bazasu tsaida haddodin Allah ba, to, babu laifi garesu cikin abindata fanshi kanta dashi, waɗancananka (hukunce-hukunce) haddodin Allah, ne, kadaku ,ƙetareta, duk wanda ya ƙetare haddodin Allah to, wadancananka sune azzalumai.

228. In ya saketa bayan biyun nan, to, ba a halatta gareshi bayan shika na'uku, saita auri wani mijin bashi ba. (ya take ta, to, idan miji na biyu ya sake ta,) to, babu laifi a gareku (matar da mijin farko,) su kuma aure (bayan ƙarewar idda,) in sun zaci sa tsaida iyakokin Allah. Wadancananka haddodin Allah ne, yana bayyanata ga mutane dasuke da sani.

وَإِذَا طَلَّقْتُمُ النِّسَآءَ فَبَلَغْنَ أَجَلَهُنَّ فَأَمْسِكُوهُنَّ بِمَعْرُوفٍ
أَوْ سَرِّحُوهُنَّ بِمَعْرُوفٍ وَلَا تُمْسِكُوهُنَّ ضِرَارًا لِّتَعْتَدُوا وَمَنْ يَّفْعَلْ
ذَٰلِكَ فَقَدْ ظَلَمَ نَفْسَهُۥ وَلَا تَتَّخِذُوا ءَايَٰتِ اللَّهِ هُزُؤًا وَاذْكُرُوا نِعْمَتَ
اللَّهِ عَلَيْكُمْ وَمَا أَنزَلَ عَلَيْكُم مِّنَ الْكِتَٰبِ وَالْحِكْمَةِ
يَعِظُكُم بِهِۦ وَاتَّقُوا اللَّهَ وَاعْلَمُوا أَنَّ اللَّهَ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمٌ ﴿229﴾
وَإِذَا طَلَّقْتُمُ النِّسَآءَ فَبَلَغْنَ أَجَلَهُنَّ فَلَا تَعْضُلُوهُنَّ أَنْ يَّنكِحْنَ
أَزْوَاجَهُنَّ إِذَا تَرَاضَوْا بَيْنَهُم بِالْمَعْرُوفِ ذَٰلِكَ يُوعَظُ بِهِۦ مَن
كَانَ مِنكُمْ يُؤْمِنُ بِاللَّهِ وَالْيَوْمِ الْآخِرِ ذَٰلِكُمْ أَزْكَىٰ لَكُمْ وَأَطْهَرُ
وَاللَّهُ يَعْلَمُ وَأَنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴿230﴾ * وَالْوَٰلِدَٰتُ يُرْضِعْنَ أَوْلَٰدَهُنَّ
حَوْلَيْنِ كَامِلَيْنِ لِمَنْ أَرَادَ أَن يُتِمَّ الرَّضَاعَةَ وَعَلَى الْمَوْلُودِ لَهُۥ رِزْقُهُنَّ
وَكِسْوَتُهُنَّ بِالْمَعْرُوفِ لَا تُكَلَّفُ نَفْسٌ إِلَّا وُسْعَهَا لَا تُضَآرَّ وَٰلِدَةٌ
بِوَلَدِهَا وَلَا مَوْلُودٌ لَّهُۥ بِوَلَدِهِۦ وَعَلَى الْوَارِثِ مِثْلُ ذَٰلِكَ فَإِنْ أَرَادَا
فِصَالًا عَن تَرَاضٍ مِّنْهُمَا وَتَشَاوُرٍ فَلَا جُنَاحَ عَلَيْهِمَا وَإِنْ أَرَدتُّمْ
أَن تَسْتَرْضِعُوا أَوْلَٰدَكُمْ فَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ إِذَا سَلَّمْتُم مَّا ءَاتَيْتُم
بِالْمَعْرُوفِ وَاتَّقُوا اللَّهَ وَاعْلَمُوا أَنَّ اللَّهَ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿231﴾

رُبُع

(LADABAN SHIKA DA MA'AMALAR ABAR SAKI)

229. Idan kunsaki mataye suka kusanci ƙarewar iddarsu, to, ku riƙesu da abin sani (a shari'a bada cutarwa ba,) koku sakesu da abin sani (a shari'a) kadaku ,barsu sai iddarsu ta cika kadaku ,riƙesu da kome don cutarwa, don kuyi shishshigi a kansu, sabodayin fansa (da waninsa,) duka wanda ya aikata wannan haƙiƙa ya zalinci kansa, kadaku ,riƙi ayoyin Allah abar izgili (da ita) ku ambaci ni'imar Allah gareku (da Musulunci) da abinda ya saukar a gareku na daga Al-ƙur'ani da abinda yake cikinsa na daga hukunce-hukunce, yanayi muku gargaɗi dashi, (ku gode masa da aiki dashi,) kuji tsoron Allah, ku tabbata haƙiƙa Allah masanine da komai.

230. Idan kun saki mataye iddarsu ta ƙare kada kuyi musu ƙeta (watau kadaku ,hana su,) su auri mazajansu, waɗanda suka sake su, in sunyi yarjejeniya tsakaninsu da abin sani (a shari'a) wancananka (hani ga barin ƙeta) ana gargaɗi dashi ga wanda ya kasance daga gareku yabada gaskiya da Allah da Ranar Lahira, (don shine mai amfani dashi,) wancananku (barin ƙeta) shiyafi alhairi gareku yafi tsarki, Allah yasan (abinda yake cikinsa na maslaha) ku kuwa baku sani ba, (kubi umarninsa).

(BA'ALIN HUKUNCE-HUKUNCEN SHAN NONO)

231. Mahaifa su shayar da 'ya'yansu shekara biyu cikakku, ga wanda yake nufin cikakken shayar da nono, wajibi ne bisa ga wanda aka yiwa haihuwa (shine uba,) ciyar dasu mahaifan nan da tufasar dasu in sun kasance aba-ban saki, da abin sani (a shari'a,) ba a kallafawa kai sai gwargwadon ikonta, kada a cuci mahaifiya saboda ɗanta, (a tilashe ta bisa shayar dashi in taƙi,) kada a cuci abin haihuwa gareshi (shine uba) saboda ɗansa (a kallafa masa fiye da ikonsa,) misalin wancananka, (abinda yake kan uba,) da uwa na tufasarwa, da ciyarwa,) ya wajabakan magajin (uba in uban ya mutu, watau jariri, ai yana kan waliyyinsa a cikin dukiyar jariri,) to, idan iyayen suka nufi yaye shi (gaban cikar shekara biyu,) daga yarjejeniya daga garesu da shawara, to, babu laifi a garesu, (a cikin wannan) idan (ku iyaye) kuka nufi ku. nemi shayar da 'ya'yanku, (ga masu shayarwa ba mahaifa ba,) to, babu laifi a gareku (a cikinsa,) idan kun miƙa abinda kuka nufi badashi garesu, (na daga lada,) da abin sani (a shari'a,) ku tsoraci Allah, ku sani haƙiƙa Allah mai ganine ga abinda kuke aikatawa.

(IDDAR MATAR DA MIJINTA YA MUTU)

وَالذِينَ يُتَوَفَّوْنَ مِنكُمْ وَيَذَرُونَ أَزْوَاجاً يَتَرَبَّصْنَ بِأَنفُسِهِنَّ
أَرْبَعَةَ أَشْهُرٍ وَعَشْراً فَإِذَا بَلَغْنَ أَجَلَهُنَّ فَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ
فِيمَا فَعَلْنَ فِي أَنفُسِهِنَّ بِالْمَعْرُوفِ وَاللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ (232)
وَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ فِيمَا عَرَّضْتُم بِهِ مِنْ خِطْبَةِ النِّسَاءِ
أَوْ أَكْنَنتُمْ فِي أَنفُسِكُمْ عَلِمَ اللَّهُ أَنَّكُمْ سَتَذْكُرُونَهُنَّ
وَلَٰكِن لَّا تُوَاعِدُوهُنَّ سِرّاً إِلَّا أَن تَقُولُوا قَوْلاً مَّعْرُوفاً
وَلَا تَعْزِمُوا عُقْدَةَ النِّكَاحِ حَتَّىٰ يَبْلُغَ الْكِتَابُ أَجَلَهُ
وَاعْلَمُوا أَنَّ اللَّهَ يَعْلَمُ مَا فِي أَنفُسِكُمْ فَاحْذَرُوهُ وَاعْلَمُوا
أَنَّ اللَّهَ غَفُورٌ حَلِيمٌ (233) * لَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ إِن طَلَّقْتُمُ النِّسَاءَ ثمن
مَا لَمْ تَمَسُّوهُنَّ أَوْ تَفْرِضُوا لَهُنَّ فَرِيضَةً وَمَتِّعُوهُنَّ
عَلَى الْمُوسِعِ قَدْرُهُ وَعَلَى الْمُقْتِرِ قَدْرُهُ مَتَاعاً بِالْمَعْرُوفِ
حَقّاً عَلَى الْمُحْسِنِينَ (234) وَإِن طَلَّقْتُمُوهُنَّ مِن قَبْلِ أَن تَمَسُّوهُنَّ
وَقَدْ فَرَضْتُمْ لَهُنَّ فَرِيضَةً فَنِصْفُ مَا فَرَضْتُمْ إِلَّا أَن يَعْفُونَ
أَوْ يَعْفُوَا الَّذِي بِيَدِهِ عُقْدَةُ النِّكَاحِ وَأَن تَعْفُوا أَقْرَبُ لِلتَّقْوَىٰ
وَلَا تَنسَوُا الْفَضْلَ بَيْنَكُمْ إِنَّ اللَّهَ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ (235)

232. Wadanda suke mutuwa daga cikinku suke barin mataye, matayen nan suyi sauraro da kawukansu (ga barin aure) wata hudu da kwana goma, (banda masu ciki su iddarsu haifewarsu, kuyanga tayi sauraro na rabin abin ambato,) to, idan muddar sauraronsu ta ƙare, to, ba laifi a gareku, (ku waliyyai) cikin abinda suka aikata a cikin kansu (na ado, da bijira ga zawarawa,) da abin sani (a shari'a,) Allah masanin (zahirin) abinda kuke aikatawa ne (da baɗininsa

(ZAWARCIN WADDA MIJINTA YA MUTU DA LADABANSA)

233. Ba laifi gareku a cikin abinda kukayi jirwaye dashi na daga zawarcin mataye waɗanda mazansu suka rasu a cikin idda (kamar ke mai kyau ce, ke mai farin jini ce, mutane da yawa suna sonki) koku ɓuye a cikin kawukanku (na nufin aurensu,) Allah yasani haƙiƙa kuda sannu zaku ringa ambaton su (da zawarci bazaku iya haƙuri ba, ya halatta muku jirwaye,) sai dai kada kuyi al-ƙawari dasu a ɓoye, amma kwa gaya musu magana abar sani (a shari'a,) shine jirwayen da aka gabatar,) kadaku ,zartar da niyyar kudurin aure sai iddata cika, ku sani haƙiƙa Allah yasan (abinda yake cikin kawukanku na zartar da niyya da waninsa) to, ku kiyaye shi, ku sani haƙiƙa Allah mai yawan gafara ne, (ga wanda ya kiyaye shi) mai jinkirin azabane (ga wanda ya cancance ta).

(ABAR SAKI GABAN DUHULI DA ABINDA YA WAJABA GARETA)

234. Babu laifi a gareku in kun saki mataye matukar bakuyi jima'i dasubako baku yanka musu sadaki ba, (ba laifi gareku cikin saki, ku sake su) ku jiyar dasu daɗi, bisa mawadaci daga gareku gwargwadonsa, bisa matalauci gwargwadonsa, daɗaɗawa da abin sani (a shari'a,) an tabbatar dashi tabbatarwa ga masu kyakkyawan aiki, (watau kubasu ɗan wani abu gwargwadon ikonku).
235. Idan kun sakesu tun gaban bakuyijima' i dasuba alhali haƙiƙa kun yanka musu sadaki, to, rabin abinda kuka yanka musu na garesu, sai ko in su matayen nan sun yi rangwame (suka bar shi,) ko wanda ragamar ƙudurin aure take hannunsa (miji ko waliyyi, sai abar mata duka ko abar masa,) kuyi rangwame shine yafi kusa ga tsoron Allah, kar ku mance fifiko tsakaninku (watau sashi yayiwa sashi karimci) haƙiƙa Ubangiji mai ganine ga abinda kuke aikatawa.

(HABA-HABADA SALLAH)

حَٰفِظُواْ عَلَى ٱلصَّلَوَٰتِ وَٱلصَّلَوٰةِ ٱلْوُسْطَىٰ وَقُومُواْ لِلَّهِ
قَٰنِتِينَ ﴿236﴾ فَإِنْ خِفْتُمْ فَرِجَالًا أَوْ رُكْبَانًا فَإِذَا أَمِنتُمْ
فَاذْكُرُواْ ٱللَّهَ كَمَا عَلَّمَكُم مَّا لَمْ تَكُونُواْ تَعْلَمُونَ ﴿237﴾
وَٱلَّذِينَ يُتَوَفَّوْنَ مِنكُمْ وَيَذَرُونَ أَزْوَٰجًا وَصِيَّةٌ لِّأَزْوَٰجِهِم
مَّتَٰعًا إِلَى ٱلْحَوْلِ غَيْرَ إِخْرَاجٍ فَإِنْ خَرَجْنَ
فَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ فِي مَا فَعَلْنَ فِي أَنفُسِهِنَّ مِن مَّعْرُوفٍ
وَٱللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿238﴾ وَلِلْمُطَلَّقَٰتِ مَتَٰعٌ بِٱلْمَعْرُوفِ
حَقًّا عَلَى ٱلْمُتَّقِينَ ﴿239﴾ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمْ ءَايَٰتِهِ
لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿240﴾ * أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ خَرَجُواْ مِن
دِيَٰرِهِمْ وَهُمْ أُلُوفٌ حَذَرَ ٱلْمَوْتِ فَقَالَ لَهُمُ ٱللَّهُ
مُوتُواْ ثُمَّ أَحْيَٰهُمْ إِنَّ ٱللَّهَ لَذُو فَضْلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ
وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَشْكُرُونَ ﴿241﴾ وَقَٰتِلُواْ فِي سَبِيلِ
ٱللَّهِ وَٱعْلَمُواْ أَنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿242﴾ مَّن ذَا ٱلَّذِي يُقْرِضُ
ٱللَّهَ قَرْضًا حَسَنًا فَيُضَٰعِفَهُۥ لَهُۥٓ أَضْعَافًا كَثِيرَةً
وَٱللَّهُ يَقْبِضُ وَيَبْصُطُ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿243﴾

رُبْع

236. Kuyi haba-haba a kan salloli (watau ku bada ita a cikin lokatanta tareda hakkokinta,) da sallah matsakaiciya, (La'asar ko Asuba, ko Azahar, ko waninsu,) ku mike don Allah (a cikin sallah) masu biyayya.

237. To, idan kukaji tsoro (na magauci, ko zaki ko kawowar kogi,) to, kuyi sallah a tafe, ko a haye, (da duban Al-kibla ko babu, ai nuni da ruku'i da sajada,) to, idan kun amince (daga tsoro, to, ku ambaci Allah, (ai kuyi sallah) kamar yadda yasanar daku abinda baku kasance kun sani ba.

(HAKKIN WACCE MIJINTA YA RASU')

238. Wadanda suke rasuwa daga cikinku suke barin mataye, to, suyi wasiyyaga matayensujiyarwa dadi (ciyarwa da tufasarwa) izuwa cikar shekara, batareda fitar.dasuba in suKafita don kansu, to, babu laifi a gareku,(ku waliyyan matacce,) a cikin abinda suka aikata a cikin kawukansu na abin sani (a shari'a,ado da barin takaba, da takaba,da rashin ci dasu,) Allah mabuwayi ne (a cikin mulkinsa,) gwanine (cikin aikinsa. An shafe tada ayar gado, jinkirin shekara kuma an shafe shi da ayar wata hudu da kwana goma).

239. Jiyarwa dadi ya tabbata ga ababan saki da abin sani (a shari'a,) an tabbata shi tabbatarwa ga masu tsoron Allah.

240. Kamar yadda Allah ya bayyana muku abinda aka ambata, yake bayanin ayoyinsa gareku don hakika kuyi amfani da hankalinku.

(GUDUN KADDARA SHINE GUZURIN TADDA ITADA KARFAFA RAN MUMINAI A KAN YAKI)

241. Yanzu bakai duba ba izuwa wadannan da suKafita daga gidaddajinsu alhali suna dubbai,don tsoron mutuwa? (Wadansu mutane ne na Bani' isra'ila annobata abku a garinsu, suka gudu) sai Ubangiji yace (dasu) "ku mutu" (suka mutu) sannan ya raya su, (bayan kwana takwas).Hakika Ubangiji mai falala ne bisa mutane, amma yawaicin mutane (kafirai) basa godewa Ubangiji.

242. (Abin nufi da ambaton labarin wadannan mutane karfafa zuciyar muminai a kan yaki) kuyi yaki saboda inganta addinin Allah, ku tabbata Allah mai jine (ga maganganunkuda aikinku,) masanine (da haluluwan da kuke ciki).

243. Wanene wandazai rantawa Allah (da ciyar da dukiyarsa Fisabilil Lahi,) rance kyakkyawa,(watau ya ciyar dashi don Allah bisa dadin zuciyarsa,) saboda haka Ubangiji ya nunka masa sakamako don sa, ninke-ninke masu yawa, (gwargwadon Ihlasinsa,) Ubangiji yana kuntatawar (arziki ga wanda yaga dama, don gwaji,) yana yalwatawar (arziki ga wanda yaga dama dongwaji, sa gode ko kuwa Izuwa gareshi ake komar da ku.

YAWAN RUNDUNA BASHIDA AMFANI IN BA ZUCIYA DA ZATA TSAYA TSAYUWAR DAKA)

أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلْمَلَإِ مِنۢ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ مِنۢ بَعْدِ مُوسَىٰٓ إِذْ قَالُوا۟
لِنَبِىٍّ لَّهُمُ ٱبْعَثْ لَنَا مَلِكًا نُّقَٰتِلْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ۖ
قَالَ هَلْ عَسَيْتُمْ إِن كُتِبَ عَلَيْكُمُ ٱلْقِتَالُ أَلَّا تُقَٰتِلُوا۟ ۖ
قَالُوا۟ وَمَا لَنَآ أَلَّا نُقَٰتِلَ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ وَقَدْ أُخْرِجْنَا
مِن دِيَٰرِنَا وَأَبْنَآئِنَا ۖ فَلَمَّا كُتِبَ عَلَيْهِمُ ٱلْقِتَالُ
تَوَلَّوْا۟ إِلَّا قَلِيلًا مِّنْهُمْ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌۢ بِٱلظَّٰلِمِينَ ﴿244﴾
وَقَالَ لَهُمْ نَبِيُّهُمْ إِنَّ ٱللَّهَ قَدْ بَعَثَ لَكُمْ طَالُوتَ
مَلِكًا ۚ قَالُوٓا۟ أَنَّىٰ يَكُونُ لَهُ ٱلْمُلْكُ عَلَيْنَا
وَنَحْنُ أَحَقُّ بِٱلْمُلْكِ مِنْهُ وَلَمْ يُؤْتَ سَعَةً مِّنَ ٱلْمَالِ ۚ
قَالَ إِنَّ ٱللَّهَ ٱصْطَفَىٰهُ عَلَيْكُمْ وَزَادَهُۥ بَسْطَةً فِى ٱلْعِلْمِ وَٱلْجِسْمِ ۖ
وَٱللَّهُ يُؤْتِى مُلْكَهُۥ مَن يَشَآءُ ۚ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ﴿245﴾
۞ وَقَالَ لَهُمْ نَبِيُّهُمْ إِنَّ ءَايَةَ مُلْكِهِۦٓ ثمن
أَن يَأْتِيَكُمُ ٱلتَّابُوتُ فِيهِ سَكِينَةٌ مِّن رَّبِّكُمْ
وَبَقِيَّةٌ مِّمَّا تَرَكَ ءَالُ مُوسَىٰ وَءَالُ هَٰرُونَ تَحْمِلُهُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ ۚ
إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً لَّكُمْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿246﴾

244. Bakayi duba ba izuwa manyan jama'a na daga Bani isra'ila bayan mutuwar Annabi Musa (ai izuwa ƙissarsu?) zamanin da suka fada ga wani Annabi nasu (Shamwilu,) bamu wani sarki muyi yaƙi dashi cikin inganta addinin Allah, (ya zama shugaban lamarinmu) Sai Annabi yace (dasu); "Anyaba kwakusata in an rubuta yaƙi gareku kuƙi yaƙi ba?"Suka ce"Menene garemu bazamuyi yaƙi cikin inganta addinin Allah ba, alhali haƙiƙa an fitar damu daga gidajenmu!" da' ya'ya'yanmu (Jalutu, ya ribace waɗansu ya kashe waɗansu, Ubangiji yace) "Yayin da aka wajabta yaƙi a garesu, sai suka juyaga barinsa, sai kaɗan daga garesu (sune wadanda suka haye ƙorama tareda Dalutu,) Allah masanine da azzalimai. (Shamwilu ya roƙi Ubangijinsa, saiya amsa masa ya aiko Dalutu).

245. Annabinsu yace dasu "haƙiƙa Ubangiji ya naɗa Dalutu sarki a gareku," sukace "ƙaƙa mulki zai kasance gareshi a kanmu, alhali mune mafiya cancantar mulki daga gareshi (saboda shi ba ɗan sarauta bane kuma baya daga ɗakin Annabci, hasali mashi majemi ne) ba a bashi yalwatar dukiyaba (dazai tsayar da mulkinsa da ita?) Annabin yace (dasu "Haƙiƙa Ubangiji ya zaɓeshi da mulki a kanku, yaƙara masa yalwa a cikin ilimi da jiki, (shine mafi sani a cikin Bani'isra'ila a wannan Lokaci, mafi kyansu mafi cikar halitta daga garesu,) Allah yana bada mulkinsa ga wanda yaga dama (ba mai magana,) Allah mayalwacin baiwa ne masanine (da wanda ya kamatada ita)".

246. Annabinsu yace (dasu, yayin da suka nemi shaida a kan mulkinsa,) "Haƙiƙa shaidar mulkinsa sunduƙi yazo muku (wanda hotunan Annabawa yake ciki, Allah ya saukar dashi bisa Annabi Adamu, Amalikawa shuwa Arab suka rinjaye su suka ƙwace shi, sun kasance suna kamun ƙafa dashi a kan magautansu) Ubangiji yace, "Akwai nutsuwa ga zukatanku a cikinsa daga Ubangijinku, da kingi daga abinda Annabi Musa da Annabi Haruna suka bari, (sune takalma biyu na Annabi Musa da sandansa, da rawanin Annabi Haruna suka bari, (sune takalma biyu na Annabi Musa da sandansa, da rawanin Annabi Haruna, da ma'auni na darɓa da kararrayayyun alluna) Mala'iku suna ɗauke dashi. Haƙiƙa akwai shaida gareku a kan mulkinsa cikin wancananka in kun kasance muminai". (Sai Mala'iku suka ɗauko shi tsakanin sama da ƙasa, alhali suna duba izuwa gareshi, suka ajiye shi nan ga Daluta sai suka ajiye shi nan ga Daluta sai sukayi caffa suka shiga yaƙi, suka zaɓi mutum dubu saba'in daga samarinsu).

فَلَمَّا فَصَلَ طَالُوتُ بِالْجُنُودِ قَالَ إِنَّ اللَّهَ مُبْتَلِيكُم بِنَهَرٍ
فَمَن شَرِبَ مِنْهُ فَلَيْسَ مِنِّي وَمَن لَّمْ يَطْعَمْهُ فَإِنَّهُ
مِنِّي إِلَّا مَنِ اغْتَرَفَ غَرْفَةً بِيَدِهِ فَشَرِبُوا مِنْهُ
إِلَّا قَلِيلًا مِّنْهُمْ فَلَمَّا جَاوَزَهُ هُوَ وَالَّذِينَ ءَامَنُوا مَعَهُ
قَالُوا لَا طَاقَةَ لَنَا الْيَوْمَ بِجَالُوتَ وَجُنُودِهِ
قَالَ الَّذِينَ يَظُنُّونَ أَنَّهُم مُّلَاقُوا اللَّهِ كَم مِّن فِئَةٍ
قَلِيلَةٍ غَلَبَتْ فِئَةً كَثِيرَةً بِإِذْنِ اللَّهِ وَاللَّهُ مَعَ
الصَّابِرِينَ 247 وَلَمَّا بَرَزُوا لِجَالُوتَ وَجُنُودِهِ قَالُوا
رَبَّنَا أَفْرِغْ عَلَيْنَا صَبْرًا وَثَبِّتْ أَقْدَامَنَا وَانصُرْنَا
عَلَى الْقَوْمِ الْكَافِرِينَ 248 فَهَزَمُوهُم بِإِذْنِ اللَّهِ
وَقَتَلَ دَاوُودُ جَالُوتَ وَءَاتَاهُ اللَّهُ الْمُلْكَ وَالْحِكْمَةَ
وَعَلَّمَهُ مِمَّا يَشَاءُ وَلَوْلَا دِفَاعُ اللَّهِ النَّاسَ بَعْضَهُم
بِبَعْضٍ لَّفَسَدَتِ الْأَرْضُ وَلَكِنَّ اللَّهَ
ذُو فَضْلٍ عَلَى الْعَالَمِينَ 249 تِلْكَ ءَايَاتُ اللَّهِ
نَتْلُوهَا عَلَيْكَ بِالْحَقِّ وَإِنَّكَ لَمِنَ الْمُرْسَلِينَ 250

247. Yayin da Dalutu yafito da runduna (daga Baitilmaƙdisi, (a Lokacin fatsaki ai zafin rana suka nemi ruwa daga gareshi) yace "Haƙiƙa Allah zai jarrabe kuda ƙorama, don mai biyayyaya bayyana daga gareku daga waninsa, ƙorama ce tsakanin Urdun (Jodan da Falasdinu) duka wanda yasha daga ruwan nan baya daga cikin mabiyana, wanda kuma baisha shiba, haƙiƙa shi yana cikin mabiyana, sai wanda ya kanfata, kanfata daya da hannunsa (bai ƙara a kanta ba, to, shi yana cikin mabiyana)" Sai suka sha suka cika cikinsu daga gareshi, sai ƙadan daga cikinsu. (suka taƙaita kan kanfata daya, akace Itace ta ishesu, su da dabbobinsu alhali suna dari ukuda goma sha uku,) yayin daya ƙetare, shida waɗanda suka bada gaskiya, taredashi, (masu cika cikinsu da ruwa) Sukace, "Bamu da iko ayau da Jalutu (Sarkin Barebari) da rundunarsa". Waɗanda suka tabbata haƙiƙa su zasu sadu da Allah, sukace "Da yawa jama'a ƙanƙanuwa ta rinjayi jama'a mai yawa da izinin Allah. Allah yana tareda masu haƙuri (da nasara da taimako)".

248. Yayin da suka fito ga Jalutu da rundunarsa, (sukayi sahu don yaƙi) sai sukace, "Ya Ubangijinmu! kwarara haƙuri a kanmu (watau kimsa mana haƙuri) ka tabbatar da digadiganmu (da ƙarfafa zukatanmu a kan yaƙi) ka taimakemu a kan mutane kafirai".

249. Sai suka karyasu da izinin Allah, Dauwuriu (wanda yake cikin sansanin Dalutu) ya kashe jalutu, Allah ya baiwa Dawuriu mulki (a cikin Bani'isra'ila) da Annabci. (bayan mutuwar Shamwila da Dalutu, basu taɓa haɗuwa ga ɗayagabansa ba,) yasanar dashi daga abinda yake so, (kamar yin silke da furicin tsuntsu).

(AMFANIN YAƘI)

Ba don ijewar Allah, mutane ba'alinsu da ba'ali ba, da ƙasa ta ɓaci (da rinjayen mushurikai da kashe Musulmi da rushe masallatai,) amma Allah ma'abocin falala ne ga mutane (ya ije ba'Alinsu ga ba'ali).

250. Wadancananka (ayoyi) ayoyin Allah ne muna labarta ta gareka (Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama) da gaskiya, haƙiƙa kai lallai kana daga cikin ma'aika, (raddi ga waɗanda sukace ba ma'aikine kaiba).

(DARAJOJIN ANNABAWA DA FIFITA ANNABI 'SALLALLAHU ALAIHI WA-SALLA-MA A KANSU DA DABI'AR MUTANE A CIKIN MABIYANSU)

حزب

* تِلْكَ اَ۬لرُّسُلُ فَضَّلْنَا بَعْضَهُمْ عَلَيٰ بَعْضٖ مِّنْهُم مَّن كَلَّمَ اَ۬للَّهُ
وَرَفَعَ بَعْضَهُمْ دَرَجَٰتٖ وَءَاتَيْنَا عِيسَى اَ۪بْنَ مَرْيَمَ اَ۬لْبَيِّنَٰتِ
وَأَيَّدْنَٰهُ بِرُوحِ اِ۬لْقُدُسِ وَلَوْ شَآءَ اَ۬للَّهُ مَا اَ۪قْتَتَلَ اَ۬لذِينَ مِنۢ
بَعْدِهِم مِّنۢ بَعْدِ مَا جَآءَتْهُمُ اُ۬لْبَيِّنَٰتُ وَلَٰكِنِ اِ۪خْتَلَفُواْ فَمِنْهُم
مَّنْ ءَامَنَ وَمِنْهُم مَّن كَفَرَ وَلَوْ شَآءَ اَ۬للَّهُ مَا اَ۪قْتَتَلُواْ وَلَٰكِنَّ اَ۬للَّهَ
يَفْعَلُ مَا يُرِيدُ ﴿251﴾ يَٰأَيُّهَا اَ۬لذِينَ ءَامَنُواْ أَنفِقُواْ مِمَّا رَزَقْنَٰكُم
مِّن قَبْلِ أَنْ يَّأْتِيَ يَوْمٞ لَّا بَيْعٞ فِيهِ وَلَا خُلَّةٞ وَلَا شَفَٰعَةٞ
وَالْكَٰفِرُونَ هُمُ اُ۬لظَّٰلِمُونَ ﴿252﴾ اَ۬للَّهُ لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ اَ۬لْحَيُّ اُ۬لْقَيُّومُ
لَا تَأْخُذُهُۥ سِنَةٞ وَلَا نَوْمٞ لَّهُۥ مَا فِي اِ۬لسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي اِ۬لْأَرْضِ
مَن ذَا اَ۬لذِے يَشْفَعُ عِندَهُۥ إِلَّا بِإِذْنِهِۦ يَعْلَمُ مَا بَيْنَ أَيْدِيهِمْ
وَمَا خَلْفَهُمْ وَلَا يُحِيطُونَ بِشَےْءٖ مِّنْ عِلْمِهِۦ إِلَّا بِمَا شَآءَ وَسِعَ كُرْسِيُّهُ
اُ۬لسَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضَ وَلَا يَـُٔودُهُۥ حِفْظُهُمَا وَهُوَ اَ۬لْعَلِيُّ
اُ۬لْعَظِيمُ ﴿253﴾ لَا إِكْرَاهَ فِي اِ۬لدِّينِ قَد تَّبَيَّنَ اَ۬لرُّشْدُ مِنَ اَ۬لْغَيِّ
فَمَنْ يَّكْفُرْ بِالطَّٰغُوتِ وَيُؤْمِنۢ بِاللَّهِ فَقَدِ اِ۪سْتَمْسَكَ
بِالْعُرْوَةِ اِ۬لْوُثْقَيٰ لَا اَ۪نفِصَامَ لَهَا وَاللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿254﴾

251. Wadancananka manzanni mun fifita ba'alinsu bisa ba'ali, (da keɓantarsa da daraja wacce bata kasance ga waninsa ba,) akwai daga cikinsu wanda Allah yayi zance dashi (kamar Annabi Musa,) ya ɗaukaka ba'alinsu a darajoji a kan waninsa (shine Annabi Sallallahu alaihi wasallama, an keɓance shi da gamawar kira, da cikar Annabci da fifita al'ummarsa a kan sauran al'ummai da mu'ujizozi masu ɗinbin yawa da keɓance - keɓance masu dinbin yawa, mun baiwa Annabi Isa ɗan Maryama hujjoji mabayyana, mun ƙarfafe shi da ran tsarki, (Jibrilu, yana tafiya taredashi inda duk ya tafi,) da Allah yanufi shiriyar mutane gaba ɗaya, da waɗanda suke bayansu na daga al'umma da basuyi yaƙe-yaƙe ba, bayan hujjoji sun zo musu, kai dai sun saɓa ne (saboda haka Allah yaso,) to, akwai daga cikinsu wanda ya tabbata kan imaninsa, akwai daga garesu wanda ya kafirta, da Allah yaga dama da basuyi yaƙe-yaƙe ba, sai dai Allah yana aikata abinda ya nufa ne, (yayi taufiƙi ga wanda yaga dama, ya taɓar da wanda yaga dama).

(KWADAITARWA A CIKIN CIYARWA)

252. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya! ku ciyar daga abinda muka azurta muku, (zakka da waninta, ku ciyar tun gaban rana wacce ba fansa a cikinta bata zoba, ba abokantaka baza tayi amfani, ba ceto (saida izinin Ubangiji, shine ranar Al-ƙiyama,) waɗanda suka kafirta (da Allah da abinda ya wajabta a kansu) sune azzalimai, (saboda sun aje al'amarin Allah ba a wurinsa ba).

(KIRARI GA ALLAH WANDA AYATIL- KURSI TA ƘUNSA)

253. Allah ba abin bautawa da gaskiya saishi, madauwamin wanzuwa, wanda ya tokare sammai da ƙassaida abinda yake cikinsu da ƙarfinsa.

254. Gyangyaɗi bata riƙonsa wala bacci, abinda yake sammai da ƙassai nasa ne (mallaka da halittada bauta,) ba mai ceto nan gareshi saida izininsa, yasan abinda yake gaban halitta (watau abinda suke cikinsa na al'amarin duniya) abinda da yake bayansu (na daga Lamarin Lahira,) basa kewayewa da komai daga iliminsa, (watau basu san komai badaga abubuwan dayasani,) sai dai abinda yaga damar (sanar dasushi daga cikinsa, ta wasiɗar manzanni,) Gadonsa (ko saninsa) ya yalwaci sammai da ƙassai, (ya kewaye dasu, Hadisi yace, sammai bakwai basu kasance ba a cikin Al-kursi, face kamar Dirhamomi guda bakwai da aka jefa su a cikin garkuwa,) kiyaye su, sammai da ƙassai bazai nauyayi Allah ba, shine maɗaukaki (cikin halittada rinjaye) maigirma.

(SHIGA CIKIN ADDINI DA WALITTA-KA A KAN MUTANE)

Ba tilasta cikin shiga Addini, hakika gaskiya ta bayyana daga bata, (wani Ansari ne yanufi ya tilasta dansa a bisa Musulunci saboda haka ayar ta sauta) to, wanda ya kafirtada Daguti, (watau shaiɗan da gunki) ya bada gaskiya da Allah, to, hakika ya riki igiya mai karfi, (wacce bata motsa ba bare ta tsinke), Allah mai ji ne (ga abinda ake fada, ko ake aikatawa,) masanine (dasu).

اللَّهُ وَلِيُّ الَّذِينَ ءَامَنُوا يُخْرِجُهُم مِّنَ الظُّلُمَاتِ إِلَى النُّورِ ﴿255﴾
وَالَّذِينَ كَفَرُوا أَوْلِيَاؤُهُمُ الطَّاغُوتُ يُخْرِجُونَهُم
مِّنَ النُّورِ إِلَى الظُّلُمَاتِ أُولَٰئِكَ أَصْحَابُ النَّارِ هُمْ
فِيهَا خَالِدُونَ ﴿256﴾ * أَلَمْ تَرَ إِلَى الَّذِي حَاجَّ إِبْرَاهِيمَ فِي رَبِّهِ
أَنْ ءَاتَاهُ اللَّهُ الْمُلْكَ إِذْ قَالَ إِبْرَاهِيمُ رَبِّيَ الَّذِي يُحْيِي وَيُمِيتُ
قَالَ أَنَا أُحْيِي وَأُمِيتُ قَالَ إِبْرَاهِيمُ فَإِنَّ اللَّهَ يَأْتِي بِالشَّمْسِ مِنَ
الْمَشْرِقِ فَأْتِ بِهَا مِنَ الْمَغْرِبِ فَبُهِتَ الَّذِي كَفَرَ
وَاللَّهُ لَا يَهْدِي الْقَوْمَ الظَّالِمِينَ ﴿257﴾ أَوْ كَالَّذِي مَرَّ عَلَىٰ قَرْيَةٍ
وَهِيَ خَاوِيَةٌ عَلَىٰ عُرُوشِهَا قَالَ أَنَّىٰ يُحْيِي هَٰذِهِ اللَّهُ
بَعْدَ مَوْتِهَا فَأَمَاتَهُ اللَّهُ مِائَةَ عَامٍ ثُمَّ بَعَثَهُ
قَالَ كَمْ لَبِثْتَ قَالَ لَبِثْتُ يَوْمًا أَوْ بَعْضَ يَوْمٍ
قَالَ بَل لَّبِثْتَ مِائَةَ عَامٍ فَانظُرْ إِلَىٰ طَعَامِكَ وَشَرَابِكَ
لَمْ يَتَسَنَّهْ وَانظُرْ إِلَىٰ حِمَارِكَ وَلِنَجْعَلَكَ ءَايَةً لِّلنَّاسِ
وَانظُرْ إِلَى الْعِظَامِ كَيْفَ نُنشِرُهَا ثُمَّ نَكْسُوهَا لَحْمًا
فَلَمَّا تَبَيَّنَ لَهُ قَالَ أَعْلَمُ أَنَّ اللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ﴿258﴾

ثمن

255/256. Allah mataimakin wađanda suka bada gaskiya ne, yana fitar dasu daga duffan (kafirci) izuwa hasken (imani,) wađanda suka kafirta kuwa, mataimakansu shaidan, yana fitar dasu daga hasken (imani) izuwa duffan (kafirci,) wadancananka sune 'yan wuta, su masu dauwama ne a cikinta.

(WANI ABU DAGA RU DIN KAFIRAI NA CIKIN KISSAR NAMARUDU DA ANNABI IBRAHIM A.S.)

257. Bakayi duba izuwa wanda yayi jayayya da Annabi Ibrahim a cikin Ubangijinsa, (shine Namarudu) don Allah yabashi mulki? Zamanin da Annabi Ibrahimu yace dashi, (alhali yace dashi "Waye Ubangijin da kake kiranmu izuwa gareshi?" Yace dashi) "Ubangijina wanda yake rayawa yake matarwa", yace ni ma ina rayawa ma matarwa", (Saiya kira mutum biyu ya kashe đaya yabar đaya,) Annabi Ibrahimu yace dashi (saboda yagan shi wawa ne,) "To, haƙiƙa Allah yana zuwa da rana daga Gabas, (ya kafa masa hujja mafi bayyana daga waccan) to, ka zoda ita kai đaga Yamma," to, sai wanda ya kafirta yayi ƙus'. Allah baya shiriyar azzalu-mai, (izuwa hujjar gaskiya).

(KISSAR UZAIRU ALAIHISSALAMU DA JAKINSA WACCE TA KUNSHI AYA A KAN TASHIN ALƘIYAMA DA HAUHAWA DA ILMIN YAKINI IZU-WA AINIL - YAKINI)

258. Ko kal duban wannan daya wuce a bisa alƙarya, (Baitil -maƙadisi, yana haye, a kan jaki, akwai kwandon baure lare dashi, da wani đan nannagaggen inibi, kwaf đaya, shine Uzairu,) alhali tana sarye a kan runfunan ta (yayin da Buhtanassaru ya rusa ta,) yace, "yaya Allah zai raya wađannan abubuwa bayan mutuwarsu. (Ya fađi haka yana cike da ban girma ga kuđirar Allah). Ubangiji ya matar dashi shekara đari sannan ya raya shi, (donya nuna masa kaifiyar wannan,) Ubangiji yace (dashi) "Nawa ka zauna a nan?" Yace "na zauna wuni ko ba'Alin wuni", (saboda shi yayi bacci ne farkon rana aka karɓi ransa, aka raya shi yayin fađuwar rana, saiya zaci cewa wannan ranar baccinsa ce,) sai Ubangiji yace "Bari! ka zauna shekara đari ne, yi duba izuwa abincinka (baure) da abin shanka (inabi) bai jirkita ba, (tareda tsawon zamani.) kai duba izuwa jakinka (yagan shi matacce, ƙasusuwansa tayi farifat, to, mun aikata wannan ne domin ka sani) kuma don mu sanya ka aya (kan tashin ƙiyama) ga mutane, kai duba izuwa kasusuwan jakinka, ƙaƙa muke ta rayata [1] sannan muke tufasar da ita nama, to, (sai yayi duba izuwa gareta, haƙiƙa ta đađđoru, an tufasar da ita nama, an busa rai a cikin wannan jaki ya tashi yana kukan Jaki") yayin da (wancananka) ya bayyana gareshi ƙarara, sai yace; "Na tabbata haƙiƙa Allah mai iko ne bisa komai". (Gani yakoriji).

(Kissar An-Nabi Ibrahimu Alaihissalam Ta Kunshi Bashi Ikon Raya Matacce Da Izinin Allah, Kamar Annabi Isa Alaihissalam, Hauhawa Daga Ilmtl - Yakini Izuwa Hakkul - Yakini)

1) Rayata: wataw muke hada ba'alinta izuwa ba'a li

وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِيمُ رَبِّ أَرِنِي كَيْفَ تُحْيِ الْمَوْتَىٰ قَالَ أَوَلَمْ
تُؤْمِن قَالَ بَلَىٰ وَلَٰكِن لِّيَطْمَئِنَّ قَلْبِي قَالَ فَخُذْ أَرْبَعَةً
مِّنَ الطَّيْرِ فَصُرْهُنَّ إِلَيْكَ ثُمَّ اجْعَلْ عَلَىٰ كُلِّ جَبَلٍ
مِّنْهُنَّ جُزْءًا ثُمَّ ادْعُهُنَّ يَأْتِينَكَ سَعْيًا وَاعْلَمْ أَنَّ اللَّهَ
عَزِيزٌ حَكِيمٌ (259) مَّثَلُ الَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمْوَالَهُمْ فِي سَبِيلِ اللَّهِ
كَمَثَلِ حَبَّةٍ أَنبَتَتْ سَبْعَ سَنَابِلَ فِي كُلِّ سُنبُلَةٍ مِّائَةُ حَبَّةٍ
وَاللَّهُ يُضَٰعِفُ لِمَن يَشَاءُ وَاللَّهُ وَاسِعٌ عَلِيمٌ (260) الَّذِينَ يُنفِقُونَ
أَمْوَالَهُمْ فِي سَبِيلِ اللَّهِ ثُمَّ لَا يُتْبِعُونَ مَا أَنفَقُوا مَنًّا وَلَا أَذًى
لَّهُمْ أَجْرُهُمْ عِندَ رَبِّهِمْ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ (261)
* قَوْلٌ مَّعْرُوفٌ وَمَغْفِرَةٌ خَيْرٌ مِّن صَدَقَةٍ يَتْبَعُهَا أَذًى ربع
وَاللَّهُ غَنِيٌّ حَلِيمٌ (262) يَٰأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُوا لَا تُبْطِلُوا صَدَقَٰتِكُم
بِالْمَنِّ وَالْأَذَىٰ كَالَّذِي يُنفِقُ مَالَهُ رِئَاءَ النَّاسِ وَلَا يُؤْمِنُ بِاللَّهِ
وَالْيَوْمِ الْآخِرِ فَمَثَلُهُ كَمَثَلِ صَفْوَانٍ عَلَيْهِ تُرَابٌ
فَأَصَابَهُ وَابِلٌ فَتَرَكَهُ صَلْدًا لَّا يَقْدِرُونَ عَلَىٰ شَيْءٍ
مِّمَّا كَسَبُوا وَاللَّهُ لَا يَهْدِي الْقَوْمَ الْكَٰفِرِينَ (263)

259. (Ka ambata Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama) zamanin da Annabi Ibrahimu (Alaihissalamu) yake cewa "Ubangiji! nuna mini yadda kake raya matattu, "ubangiji yace "Baka bada gaskiya (da ikona bisu rayawa) ba ne?" Yace "Na bada gaskiya, sai dai na tambayeka ne don zuciyata ta nutsu" (yadda gani yakori ji haka ɗandano yakori gani) sai Ubangiji yace "Sai ka riƙi hudu daga tsintsaye, kuma ka tattara su izuwa gareka, ka gididdibasu, ka cudanya namansu da gashinsu, sannan ka sanya yanki daga garesu, a kan kowane dutse daga duwatsun Ƙasarka. sannan ka kirawo su zuwa gareka, sa zo maka aguje, ka tabbata Ubangiji mabuwayi ne (a bisa komai.) gwanine a cikin aiki". (Saiya riƙi kumaren - gabas watau ɗawisu, da mikiya, da hankaka, da zakara, yayi musu abinda aka ce, ya riƙe kawukansu a hannunsa ya kirawo su, sai kowace tsoka ta amsa ta tafi izuwa 'yar uwarta har gangar jukkunansu ta hadu, sai suka gabato izuwa kawukansu waɗanda suke riƙe a hannun Annabi Ibrahimu Alaihissalam (ɗanɗano yakori gani).

(CIYARWA SABODA ALLAH, DA LADABANSA DA SHARUDDANSA)

260. Misalin ciyarwar waɗanda suke ciyar da dukiyoyinsu saboda Allah, tamfar misalin ƙwayace ta tsirar da zanganniya bakwai, a cikin kowace zanganniya akwai ƙwaya ɗari, (haka Allah yake ninninka musu ladan ciyarwarsu, har izuwa ninki bakwai,) Allah yana ninka lada fiye da haka ga wanda yaga dama, (gwargwadon Ihlasin mai ciyarwa,) Allah mayalwacin falala ne, masani (da wanda ya cancanci ninkawa).

261. Waɗanda suke ciyar da dukiyoyinsu saboda Allah, sannan basa gori ga wanda suka ciyar wala kwarkwara, (shine gaya wa wani alherin da akayi musu.) ladansa na garesu nan ga Ubangijin su, ba tsoro a garesu (ga abinda suka gabata) baza suyi ɓakin ciki ga abinda ya wuce ba a Lahira, (a duniya yana yiwuwa suyi bakin ciki saboda duniya gidan baƙin ciki ce).

262. Magana kyakkyawa (kamar Allah ya baka hakuri ga almajiri) da gafara (ga dan'uwanka Musulmi,) shine yafi daga sadaka, wacce gori yake bin tada kwarkwara. Allah mawadaci ne (ga barin bayinsa) mai jinkirin azabane (ga wanda ya cancan-ceta, mai kwarkwara ko waninsa).

263. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya! kadaku .ɓata ladan sadakarkuda gorlda kwarkwara, kamar ɓatawar wanda yake ciyar da dukiyarsa don riyaga mutane bai bada gaskiya da Allah da ranar lahira ba, munafiki, to, misalinsa kamar fa ce mai santsi da turbaya take kanta, mana ko ya same ta yabar ta simil, (ba komai a kanta,) basu da iko (su munafukan nan, masu ciyarwa ba don Allah ba, basu da iko) bisa wani abu da suka aikata, ai bazasu sami ladansa ba a Lahira, kamar yadda ba a sanii komai na turɓaya a kanta ba saboda ruwa ya tafi dashi,) AUah baya shiryar da mulane kafirai.

(MISALIN WANDA YAKE CIYARWA DON ALLAH DA WANDA YAKE CIYARWA BA DON ALLAH BA)

وَمَثَلُ اُ۬لذِينَ يُنفِقُونَ أَمْوَٰلَهُمُ اُ۪بْتِغَآءَ مَرْضَاتِ اِ۬للَّهِ
وَتَثْبِيتاً مِّنْ أَنفُسِهِمْ كَمَثَلِ جَنَّةٍ بِرُبْوَةٍ أَصَابَهَا وَابِلٌ
فَـَٔاتَتْ أُكْلَهَا ضِعْفَيْنِ فَإِن لَّمْ يُصِبْهَا وَابِلٌ فَطَلٌّ
وَاللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ (264) أَيَوَدُّ أَحَدُكُمُ أَن تَكُونَ
لَهُۥ جَنَّةٌ مِّن نَّخِيلٍ وَأَعْنَابٍ تَجْرِے مِن تَحْتِهَا اَ۬لْأَنْهَٰرُ لَهُۥ فِيهَا
مِن كُلِّ اِ۬لثَّمَرَٰتِ وَأَصَابَهُ اُ۬لْكِبَرُ وَلَهُۥ ذُرِّيَّةٌ ضُعَفَآءُ
فَأَصَابَهَا إِعْصَارٌ فِيهِ نَارٌ فَاحْتَرَقَتْ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ
اُ۬للَّهُ لَكُمُ اُ۬لْءَايَٰتِ لَعَلَّكُمْ تَتَفَكَّرُونَ (265) * يَٰٓأَيُّهَا اَ۬لذِينَ ثمن
ءَامَنُوٓاْ أَنفِقُواْ مِن طَيِّبَٰتِ مَا كَسَبْتُمْ وَمِمَّآ أَخْرَجْنَا لَكُم
مِّنَ اَ۬لْأَرْضِ وَلَا تَيَمَّمُواْ اُ۬لْخَبِيثَ مِنْهُ تُنفِقُونَ وَلَسْتُم
بِـَٔاخِذِيهِ إِلَّآ أَن تُغْمِضُواْ فِيهِ وَاعْلَمُوٓاْ أَنَّ اَ۬للَّهَ غَنِيٌّ حَمِيدٌ (266)
اِ۬لشَّيْطَٰنُ يَعِدُكُمُ اُ۬لْفَقْرَ وَيَأْمُرُكُم بِالْفَحْشَآءِ
وَاللَّهُ يَعِدُكُم مَّغْفِرَةً مِّنْهُ وَفَضْلاً وَاللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ (267)
يُؤْتِے اِ۬لْحِكْمَةَ مَن يَشَآءُ وَمَن يُؤْتَ اَ۬لْحِكْمَةَ
فَقَدُ اُوتِيَ خَيْراً كَثِيراً وَمَا يَذَّكَّرُ إِلَّآ أُوْلُواْ اُ۬لْأَلْبَٰبِ (268)

264. Misalin ciyarwar wadanda suke ciyar da dukiyoyinsu don neman yardar Allah da tabbatar da sakamako a kansa daga kaw-ukansu, (sabanin munafukai wadanda basa ƙaunar sakamakon Allah) kamar gona ce a tudun jigawa mana ko ya same ta, ta bada amfanin cikinta ninki biyu (na amfanin waninta) idan mana ko bai same ta ba, to yayyafi. (bata bukatar yawan ruwa saboda kyanta, to, haka ciyarwar mai Ihlasi take ƙaruwa gunn Allah ta yawaita ko ta ƙaranta.) Allah mai ganine da abindaku ,ke aikatawa.

265. Yanzu dayanku yana gurin; cewa yana da gona ta dabmai da inabai, ƙoramu tana kwarara ƙarkashinta, yana da dukkan 'ya'yan itaciya a cikinta, alhali tsufa ya riske shi, yana da zurriya raunana (da basu da ikon aikata ta,) kuma guguwa ta same ta, da wuta take cikinta, ta ƙone ƙurmus (ya rasa amfaninta a lokacin dayafi bukatuwa izuwa gareta, kuma ya wanzu shi da 'ya'yansa gajiyayyu, dimau-tattu basu da katabis, wannan misali ne ga mai ciyarwa ba don Allah ba, da rashin amfaninta Lokacin dayafi bukatarta a lahira). Irin yadda Allah yayi muku bayanin abinda aka ambata, yake bayanin ayoyinsa, don hakika kuyi amfani da hankalinku a cikin tunani.

(WANI ABU DAGA ABINDA AKE CIYARWA DAGA GARESHI DA KAMANNINSA)

266. Yaku wadandaku ,ka bada gaskiya! ku ciyar daga dadadan abindaku, ka tsuwurwurta na dukiya, ku ciyar kuma daga dadadan abinda muka fitar daga ƙasa don ku, (na ƙwayika da 'ya'yan itatuwa,) kada ku nufi komabaya, ku ciyar daga cikin sa (zakka ko waninta,) bako zaku ƙarbe shi ba (in an bakushi i cikin haƙƙinku) sai in kun rimt se ido a cikinsa, (watau baza ki karbe shi ba saida kyar,) ku sani Allah mawadaei ne (ga bai in ciyarwarku,) abin godewa ne (bisa kowane hali).

(SHAIDAN DA CIYARWA)

267. Shaidan yana baku tsoro da talauci in kun yi sadaka, yana umarninkuda alfasha, (kamar hana zakka da wanin ta,) Allah yanayi muku alkawarin gafara (zunubanku) daga gareshi da sakamako (daga gareshi,) Allah mayalwacin lalala ne, masaninc (da wanda ya ciyar don sa).

(ILMIMAIAMFANI)

268. Allah yana bada hikima (watau ilmi mai amfani wanda yake kaiwa ga aiki dashi) ga wanda yaga dama, wanda aka bashi ilmi mai amfani, haƙiƙa an bashi alheri mai yawa, ba kowa ke wa'azantuwa ba, sai ma'abota hankula.

(WANI ABU DAGA HUKUNCENHU-KUNCEN CIYARWA HAR YAU)

وَمَا أَنفَقْتُم مِّن نَّفَقَةٍ أَوْ نَذَرْتُم مِّن نَّذْرٍ فَإِنَّ
اللَّهَ يَعْلَمُهُ وَمَا لِلظَّالِمِينَ مِنْ أَنصَارٍ ﴿269﴾ إِن تُبْدُوا
الصَّدَقَاتِ فَنِعِمَّا هِيَ وَإِن تُخْفُوهَا وَتُؤْتُوهَا الْفُقَرَاءَ
فَهُوَ خَيْرٌ لَّكُمْ وَنُكَفِّرْ عَنكُم مِّن سَيِّئَاتِكُمْ
وَاللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ ﴿270﴾ * لَّيْسَ عَلَيْكَ هُدَاهُمْ
وَلَكِنَّ اللَّهَ يَهْدِي مَن يَشَاءُ وَمَا تُنفِقُوا مِنْ خَيْرٍ
فَلِأَنفُسِكُمْ وَمَا تُنفِقُونَ إِلَّا ابْتِغَاءَ وَجْهِ اللَّهِ
وَمَا تُنفِقُوا مِنْ خَيْرٍ يُوَفَّ إِلَيْكُمْ وَأَنتُمْ
لَا تُظْلَمُونَ ﴿271﴾ لِلْفُقَرَاءِ الَّذِينَ أُحْصِرُوا فِي سَبِيلِ اللَّهِ
لَا يَسْتَطِيعُونَ ضَرْبًا فِي الْأَرْضِ يَحْسِبُهُمُ الْجَاهِلُ
أَغْنِيَاءَ مِنَ التَّعَفُّفِ تَعْرِفُهُم بِسِيمَاهُمْ لَا يَسْأَلُونَ
النَّاسَ إِلْحَافًا وَمَا تُنفِقُوا مِنْ خَيْرٍ فَإِنَّ
اللَّهَ بِهِ عَلِيمٌ ﴿272﴾ الَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمْوَالَهُم بِاللَّيْلِ
وَالنَّهَارِ سِرًّا وَعَلَانِيَةً فَلَهُمْ أَجْرُهُمْ عِندَ
رَبِّهِمْ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿273﴾

ربع

269. Duk abindaku ,ka ciyar na abin ciyarwa (zakka ko waninta,) koku kayi alwashi na daga abin alwashi (ku ka cika dashi,) to, hakika Allah yasan shi, azzalimai kuwa (da hana zakka ko ƙin cika alwashi to ƙin alheri) basu da mai hana musu azabar Ubangiji.

270. Idan ku ka bayyana sadakoki (zakka ko waninta) to, madalla da ita (ai madalla da bayyana ta,) idan koku ka ɓoyeia. ku ka baiwa mabukata, to, shi yafi aintani a gareku, (daku ,bayyan-atada baiwa mawadata ita, amma sadakar tarilla bayyanata yafi don ayi koyi, don kuma a kore tuhuma, kuma tilas ne ita a baiwa maɓukatan) kuma ma kankare daga miyagun ayyukanku ga barinku, Allah inasanine da abindaku ,ke aikatawa (yasan zahirinsa da baɗininsa, ba abinda ya ɓuya a gareshi na ayyukanku).

(WADANOA AKE BA SADAKA DA BA'ALIN HUKUNCEHUKUNCENTA)

271. Shiryar dasu ba a kan ka yake ba, sai dai Allah yana shiryar da wanda yaga dama ne, duk abinda zaku ciyar na daga dukiya to, ga kawukanku ne, kadaku ,ciyar sai don neman yardar Allah, duk abindaku ,ka ciyar na dukiya za a cika muku sakamakonsa, baza a tauye muku komai ba.

(AHLIL - SUFFATI WATAU SUFAYE NA ZAMANIN ANNABI
SALLALLA-HU ALAIHI WA SALLAMA)

272. Sadaka ta tabbata ga fuƙara'u waɗanda suka tsare kawukansu a kan yaƙi (sune Ahlis - suffati, su arbaminya ne na muhajirai. an dakatar dasu saboda neman karatun Alƙur'ani da sallah bayan Annabi (Sallallahu alaihi wasallama da kiyamillaili da fita yaƙi,) basu da damar tafiya don ciniki da neman abinci a cikin ƙasa (saboda sun shagala dayaki,) wanda hai san halinsu ba yana zaton su mawadata ne, saboda kamun kai, basa rokon kowa wani abu, kana saninsuda alamarsu (shine tawali'u da alamar jikkata,) basa tambayar kowa wani abu, bare suyi naci, duk abindaku ,ka ciyar na du-kiya Allah masanine dashi.

273. Waɗanda suke ciyar da dukiyoyinsu, dare da rana, a asirce da bayyane, to, ladansu na garesu nan ga Ubangijinsu, ba tsoro a garesu, su baza suyi baƙin ciki (a lahira) ba.

(RIBADA HADARINTA GA MA-CIYINTADA SAURAN AL'UMMA)

ٱلَّذِينَ يَأْكُلُونَ ٱلرِّبَوٰاْ لَا يَقُومُونَ إِلَّا كَمَا يَقُومُ ٱلَّذِي
يَتَخَبَّطُهُ ٱلشَّيْطَٰنُ مِنَ ٱلْمَسِّ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ قَالُوٓاْ
إِنَّمَا ٱلْبَيْعُ مِثْلُ ٱلرِّبَوٰاْ وَأَحَلَّ ٱللَّهُ ٱلْبَيْعَ وَحَرَّمَ ٱلرِّبَوٰاْ فَمَن جَآءَهُۥ
مَوْعِظَةٌ مِّن رَّبِّهِۦ فَٱنتَهَىٰ فَلَهُۥ مَا سَلَفَ وَأَمْرُهُۥٓ إِلَى ٱللَّهِ
وَمَنْ عَادَ فَأُوْلَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿274﴾
يَمْحَقُ ٱللَّهُ ٱلرِّبَوٰاْ وَيُرْبِي ٱلصَّدَقَٰتِ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ كُلَّ كَفَّارٍ أَثِيمٍ ﴿275﴾
إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُاْ
ٱلزَّكَوٰةَ لَهُمْ أَجْرُهُمْ عِندَ رَبِّهِمْ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿276﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَذَرُواْ مَا بَقِيَ مِنَ ٱلرِّبَوٰاْ
إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿277﴾ فَإِن لَّمْ تَفْعَلُواْ فَأْذَنُواْ بِحَرْبٍ مِّنَ ٱللَّهِ
وَرَسُولِهِۦ وَإِن تُبْتُمْ فَلَكُمْ رُءُوسُ أَمْوَٰلِكُمْ لَا تَظْلِمُونَ
وَلَا تُظْلَمُونَ ﴿278﴾ وَإِن كَانَ ذُو عُسْرَةٍ فَنَظِرَةٌ إِلَىٰ
مَيْسَرَةٍ وَأَن تَصَدَّقُواْ خَيْرٌ لَّكُمْ إِن كُنتُمْ
تَعْلَمُونَ ﴿279﴾ وَٱتَّقُواْ يَوْمًا تُرْجَعُونَ فِيهِ إِلَى ٱللَّهِ
ثُمَّ تُوَفَّىٰ كُلُّ نَفْسٍ مَّا كَسَبَتْ وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿280﴾

274. Wađanda suke cin riba, (shine kari a cikin mu'amala, na kuđi ko ajali, a kuđi ko a abinci) bazasu tashi (daga kabarinsu) ba, sai dai kamar (tashin) wanda Shaiđan yake bige shi saboda hauka, wannan abinda ya same su, saboda su sunce; "Shi dai ciniki kawai kamar riba ne" (watau halaliyace, Ubangiji yayi musu raddi yace); "Allah ya halatta ciniki, ya haramta riba," to, wanda gargađi, yazo masa daga Ubangijinsa, ya hanu (ga barin cin riba,) to, abinda ya wuce gaban hani ya halatta a gareshi, lamarinsa (a cikin afwa) yana ga Allah. wađanda suka koma kuwa (izuwa cin riha, da kwatanta shi a ciniki a halacci,) to, wađancananka 'yan wuta ne su masu dauwama ne a cikinta.

275. Allah yana shafe wa riba albarka yana ƙara sadake - sadake (yanayi mata albarka yana ninninka sakamakonta,) Allah ba yason dukkan kafiri, (da halatta riba,) fajiri (da cin ta).

276. Wađanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagari suka tsayar da sallah suka bada zakka ladansu na garesu nan ga Ubangijinsu, ba tsoro a garesu,su baza suyi baƙin ciki (a ranar Lahira) ba.

277. ya wadanđa suka bada gaskiya! kuji tsoron Allah, ku bar abinda ya ragu na daga riba, in kun kasance muminai.

278. Iđan baku aikata abinda aka umarce ku dashi ba, to, kuyi sani dayakin Allah dana ma'aikinsa, (wannan barazana ce daga Allah, sai Sahabbai sukace "Wane mu da wannan yaƙi,") idan kun tubadaga gareshi, to, asalan dukiyoyinku na gareku bazakuyi zalunci (da ƙari) ba, baza a zalince ku (da ragi) ba.

279. Idan mabarci ma'abocin wuyar ƙudi ya samu to, sai kuyi masa sauraro izuwa sauƙi, kuyi sadaka (a gareshi da kuđin daku ,ke bin sa) (watau ku saryar masa shi yafi amfani a gare ku, in kun kasance kun san haka ya fi, (to, ku aikata shi. A cikin hadisi:Wanda ya saurarawa mawuyacin kudi, ko ya rage masa, Allah ya inuwance shi a cikin inuwarsa, ranar da ba inuwa sai inuwarsa).

280. Kuji tsoron (azabar) rana, da ake komar daku ,izuwa Allah a cikinta (ranar alƙiyama,) sannan a sakawa kowace kai abindata aikata (na hairi ko sharri,) alhali su baza a zalince su ba, (da tauye hasana ko ƙarin cikin sayyi'a).

(AYAR BASHI DA MA'AMALAR YAU DA KULLUM DA BADA SHAIDA DA LADABAN MA'AMULOLI DA GAR-GADI A CIKIN TSARE GASKIYA A CIKIN KOWACE MA'AMALAR CINIKI KO WANINSA) DA BAYA NIN SHIR-YAR DA BAY, IZUWA MASLA HO-HIN DUNIYAR SU, DOMIN DUNIYA GONAR LAHIRA CE. GYARAN LAHI-RA BAZAI YIWU BA SAIDA GYARAN DUNIYA, SABODA HAKA ALLAH YAI BAYA NIN GYARAN DUNIYA DA WANNAN AYA WACCE MAFI TSAWON AYO YIN AL KUR'ANI.

ثمن

* يَٰٓأَيُّهَا اَ۬لذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا تَدَايَنتُم بِدَيْنٍ اِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمّٗى
فَاكْتُبُوهُۖ وَلْيَكْتُب بَّيْنَكُمْ كَاتِبُۢ بِالْعَدْلِۖ وَلَا يَأْبَ
كَاتِبٌ اَنْ يَّكْتُبَ كَمَا عَلَّمَهُ اُ۬للَّهُۖ فَلْيَكْتُبْ وَلْيُمْلِلِ
اِ۬لذِے عَلَيْهِ اِ۬لْحَقُّ وَلْيَتَّقِ اِ۬للَّهَ رَبَّهُۥ وَلَا يَبْخَسْ مِنْهُ شَيْـٔاۖ
فَإِن كَانَ اَ۬لذِے عَلَيْهِ اِ۬لْحَقُّ سَفِيهاً اَوْ ضَعِيفاً اَوْ لَا يَسْتَطِيعُ
أَن يُّمِلَّ هُوَ فَلْيُمْلِلْ وَلِيُّهُۥ بِالْعَدْلِۖ وَاسْتَشْهِدُواْ شَهِيدَيْنِ
مِن رِّجَالِكُمْۖ فَإِن لَّمْ يَكُونَا رَجُلَيْنِ فَرَجُلٞ وَامْرَأَتَٰنِ
مِمَّن تَرْضَوْنَ مِنَ اَ۬لشُّهَدَآءِ أَن تَضِلَّ إِحْدَىٰهُمَا فَتُذَكِّرَ إِحْدَىٰهُمَا
اَ۬لْاُخْرَىٰۖ وَلَا يَأْبَ اَ۬لشُّهَدَآءُ إِذَا مَا دُعُواْۖ وَلَا تَسْـَٔمُوٓاْ
أَن تَكْتُبُوهُ صَغِيراً اَوْ كَبِيراً اِلَىٰٓ أَجَلِهِۦۖ ذَٰلِكُمُۥٓ أَقْسَطُ عِندَ اَ۬للَّهِ
وَأَقْوَمُ لِلشَّهَٰدَةِ وَأَدْنَىٰٓ أَلَّا تَرْتَابُوٓاْ إِلَّآ أَن تَكُونَ تِجَٰرَةٌ
حَاضِرَةٞ تُدِيرُونَهَا بَيْنَكُمْ فَلَيْسَ عَلَيْكُمْ جُنَاحٌ اَلَّا تَكْتُبُوهَاۖ
وَأَشْهِدُوٓاْ إِذَا تَبَايَعْتُمْۖ وَلَا يُضَآرَّ كَاتِبٞ وَلَا شَهِيدٞۖ
وَإِن تَفْعَلُواْ فَإِنَّهُۥ فُسُوقُۢ بِكُمْۖ وَاتَّقُواْ اُ۬للَّهَۖ
وَيُعَلِّمُكُمُ اُ۬للَّهُۖ وَاللَّهُ بِكُلِّ شَےْءٍ عَلِيمٞ ۝281

281. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! idan ku kayi ma'amala ta bashi (ko sautu ko rance) izuwa ajali abin ambato, to, ku rubuta shi (don ijewa gajayayya,) marubuci ya rubuta (takardar bashi) a tsakaninku, da adalci (a cikin rubutun, kadayayi dadi a cikin dukiya da ajali kada yayi ragi,) kada mumbuci yaki rubuta irin yadda Allah yasanar dashi, ya rubuta, (don abinda aka rubuta shine ke tabbata) wanda haƙƙi ka kansa ya badashifta, (yayi furuci da abinda yake kansa,) yaji tsoron Allah Ubangijinsa (a cikin shiftar) kada ya tauye komai (daga abinda ake bin sa,) idan wanda hakkin nan yake kansa ya kasance wawa (almubazzari, ko rarrauna ga barin shifta saboda ƙanƙanta ko girma ko bashi da ikon yin shifta saboda bebantaka ko rashin sanin yare) to, waliyinsa ya badashifta, (mahaifinsa, ko wasiyinsa, ko kuma mai tafinta, ya badashiftada adalci [1], ku ka fa shaidu guda biyu) a kan wannan bashin) daga (mazajenku) balagag'gu mulsulmai' ya'ya ye, ku musulmi idan shaidun nan basu kasance mazaje biyu ba, to, mutum guda da mace biyu su shaida, ɗaga waɗandaku ,ka yarda dasu na daga shaidu (saboda addininsu da adalcinsu, amfanin mata biyu a shaida) saboda in daya ta mance (shaidar) to, daya wacce bata mance bata tinawa daya (wacce ta mance,) kada shaidu su ƙi idan an kirawo su (izuwa daukar shaida ko bada ita,) kadaku ,ƙosa daga rubuta haƙƙin daku ,ka ki shaida a kansa, (saboda yawan abukuwa,) ƙanƙane ne (haƙƙin) ko mai yawa, izuwa ajalinsa.Wannan rubutawa shi yafi adalci nan ga Allah, (saboda abinda aka haddace bakasafai yake zama ba) shine yafi daidai ga shaida, (don shine maganin mantuwa,) shine kuma yafi kusa izuwa baza ayi kokonto (a cikin gwarg-wadon haƙƙi ko ajali ba,) sai ko idan ta zama ciniki mahalarciya (ta yau da kullum,) ku ke ma'amala da ita a tsakaninku, (wacce baku rubuta wani ajali ba,) to, ba laifi a gareku in baku rubuta ta ba, ku shaidar idan kun yi ma'amala ta ciniki (saboda shine yafi ije saɓani,) kada a cuci marubuci (da a kallafa masa ya rubuta abinda bai kamata a kallafa masa ya nibuta ba,) kada a cuci shaida (da a kallafa masa ya shaidar da abinda bai kamata, ya shaidar ba.) to, idan ku ka aikata (abinda aka hane ku ga barinsa,) to, wannan (aikata wannan) fasiƙanci ne a gareku, (watau tawaye ne ga Allah,) kuji tsoron Allah (a cikin amru da nahyu). Allah yana sanar daku ,(masalahohin al'amarinku, Allah masanine da komai.

(HALACCIN JINGINA DA LADABANTA)

1) Adalci manyaj

رُبع

* وَإِن كُنتُمْ عَلَىٰ سَفَرٍ وَلَمْ تَجِدُواْ كَاتِبًا فَرِهَٰنٌ مَّقْبُوضَةٌ
فَإِنْ أَمِنَ بَعْضُكُم بَعْضًا فَلْيُؤَدِّ الَّذِي اؤْتُمِنَ أَمَٰنَتَهُۥ وَلْيَتَّقِ اللَّهَ
رَبَّهُۥ وَلَا تَكْتُمُواْ الشَّهَٰدَةَ وَمَن يَكْتُمْهَا فَإِنَّهُۥ ءَاثِمٌ قَلْبُهُۥ
وَاللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ عَلِيمٌ ﴿282﴾ لِّلَّهِ مَا فِي السَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ
وَإِن تُبْدُواْ مَا فِي أَنفُسِكُمْ أَوْ تُخْفُوهُ يُحَاسِبْكُم بِهِ اللَّهُ
فَيَغْفِرُ لِمَن يَشَاءُ وَيُعَذِّبُ مَن يَشَاءُ وَاللَّهُ عَلَىٰ
كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ﴿283﴾ ءَامَنَ الرَّسُولُ بِمَا أُنزِلَ إِلَيْهِ مِن رَّبِّهِۦ
وَالْمُؤْمِنُونَ كُلٌّ ءَامَنَ بِاللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ
وَرُسُلِهِۦ لَا نُفَرِّقُ بَيْنَ أَحَدٍ مِّن رُّسُلِهِۦ وَقَالُواْ
سَمِعْنَا وَأَطَعْنَا غُفْرَانَكَ رَبَّنَا وَإِلَيْكَ الْمَصِيرُ ﴿284﴾
لَا يُكَلِّفُ اللَّهُ نَفْسًا إِلَّا وُسْعَهَا لَهَا مَا كَسَبَتْ وَعَلَيْهَا مَا اكْتَسَبَتْ
رَبَّنَا لَا تُؤَاخِذْنَا إِن نَّسِينَا أَوْ أَخْطَأْنَا رَبَّنَا وَلَا تَحْمِلْ
عَلَيْنَا إِصْرًا كَمَا حَمَلْتَهُۥ عَلَى الَّذِينَ مِن قَبْلِنَا
رَبَّنَا وَلَا تُحَمِّلْنَا مَا لَا طَاقَةَ لَنَا بِهِۦ وَاعْفُ عَنَّا وَاغْفِرْ لَنَا
وَارْحَمْنَا أَنتَ مَوْلَىٰنَا فَانصُرْنَا عَلَى الْقَوْمِ الْكَٰفِرِينَ ﴿285﴾

282. In kun kasance matafiYaku kayi bashi baku sami marubuci ba, to, sai a karbi jingina (hadisi ya bayyana cewa jingina halal ce koda a zaman gida) idan ba'alin ku ya amince da ba'all, (watau mai bada bashiya amince da mabarci, bai karbi jingina daga gunsa ba,) to, mabarcin nan ya biya bashin nan nasa, yaji tsoron Allah Ubangijinsa (a cikin biya) kadaku ,ɓoyé shaida idan an kira ku dan a kafa ku shaidu,) wanda ya ɓoye shaida kuwa ƙaƙiƙa shi zuciyarsa mai zinibi ce. Allah masanine da abindaku ,ke aikatawa.

(KEWAYEWAR SANIN ALLAH DA CIKAKKEN MULKINSA DA IKONSA)

283. Abinda yake cikin sammai da kassaina Ubangiji ne, in ku ka bayyana abinda yake cikin zuciyarku, (na daga mummuna da zartar da niyya a kansa) koku ka ɓoye, Allah zai rike ku dashi (ranar Alƙiyama, in ku ka aikata shi koku ka zartar da niyyar aikata shi) yayi gafara ga wanda yaso, yayi azaba ga wanda yaso, Allah mai iko ne bisa komai.

(MUMINAI WAƊANDA SUKE MA-GASGATA A IMANI DA ADDU'ARSU DA RASHIN BAMBANCI TSAKANIN VIANZANNI, HAKA MA WALIYYAI)

284. Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) yagasgatada abinda aka saukar izuwa gareshi daga Ubangijinsa (Alƙur'ani,) haka ma muminai (dukkansu) sun gasgatada Allah da Mala'ikunsa, da Littatta-fansa, da Manzanninsa, suna cewa "Barna rarrabewa tsakanm daya daga manzanninsa" (mu bada gaskiya da ba'ali, mu kafircc da ba'ali; waliyyai ma haka, saboda hadis yace kowane waliyyi a kan dunduniyar Annabi yake) suka ce; "Munji (abinda ka umarce mu dashi jin karba) mun bi, muna roƙanka gafarar ka ya Ubangijinmu! izuwa gareka ne komawarmu".

285. Allah baya kallafawa kai sai ikonta (ta sauka yayin da muminai suka kai karar wusuwasi suka tsoraci riƙo a kansa) abindata aikata (na alheri) na gareta, abindata aikata (na shairi) yana kanta, (ba a kama wani da laifin wani, wala da abinda bai aikata ba, shine abinda yayi wasiwasi dashi a ransa na hajisi da hadiri da hadisin nafsi da hammu, ku cc) "Ya Ubangijin-mu kadaka riƙe mu in mun mance ko munyi kuskure, Ya Ubangijinmu, kadaka ɗora nauyi a kannu tamfar daka dora shi a bisa waɗanda suke gabanmu, (Bani'isra'ila,kashe kai a cikin tuba, fitar da rubu'in duklya a cikin zakka, yanke gurin da najasa ta taɓa ajiki ko a tufafi), Ya Ubangijinmun, kadaka dora mana abinda bamu da iko dashi (na taklifi da bala'i,) kayi rangwame garemu (da shafe zunubanmu) kayi mana gafara, kayi manajinkai, kaine shugabanmu, sai ka taimake mu a kan mutane kafirai" (da tsayar da hujja da galaba a cikin yakinsu, don sha'anin shugabane taimakon bayinsa a kan magauta. A cikin hadisi yayin da wannan aya ta sauka Annabi Sallallahu alaihi wasallama ya karanta ta, sai akace dashi ƙarshen kowace kalma, haƙiƙa na amsa).

سُورَةُ آلِ عِمْرَانَ مَدَنِيَّةٌ 3

وَهِيَ مِائَتَا آيَةٍ 200

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

الٓمٓ ۝ اللَّهُ لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ الْحَيُّ الْقَيُّومُ ۝1 نَزَّلَ عَلَيْكَ الْكِتَٰبَ بِالْحَقِّ
مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ وَأَنزَلَ التَّوْرَىٰةَ وَالْإِنجِيلَ ۝2 مِن قَبْلُ
هُدًى لِّلنَّاسِ وَأَنزَلَ الْفُرْقَانَ ۝3 إِنَّ الَّذِينَ كَفَرُوا بِـَٔايَٰتِ اللَّهِ لَهُمْ
عَذَابٌ شَدِيدٌ وَاللَّهُ عَزِيزٌ ذُو انتِقَامٍ ۝4 * إِنَّ اللَّهَ لَا يَخْفَىٰ عَلَيْهِ شَيْءٌ
فِي الْأَرْضِ وَلَا فِي السَّمَآءِ ۝5 هُوَ الَّذِي يُصَوِّرُكُمْ فِي الْأَرْحَامِ كَيْفَ
يَشَآءُ لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ ۝6 هُوَ الَّذِي أَنزَلَ عَلَيْكَ الْكِتَٰبَ
مِنْهُ ءَايَٰتٌ مُّحْكَمَٰتٌ هُنَّ أُمُّ الْكِتَٰبِ وَأُخَرُ مُتَشَٰبِهَٰتٌ فَأَمَّا الَّذِينَ
فِي قُلُوبِهِمْ زَيْغٌ فَيَتَّبِعُونَ مَا تَشَٰبَهَ مِنْهُ ابْتِغَآءَ الْفِتْنَةِ وَابْتِغَآءَ تَأْوِيلِهِ
وَمَا يَعْلَمُ تَأْوِيلَهُ إِلَّا اللَّهُ وَالرَّٰسِخُونَ فِي الْعِلْمِ يَقُولُونَ ءَامَنَّا بِهِ كُلٌّ مِّنْ
عِندِ رَبِّنَا وَمَا يَذَّكَّرُ إِلَّا أُولُوا الْأَلْبَٰبِ ۝7 رَبَّنَا لَا تُزِغْ قُلُوبَنَا بَعْدَ
إِذْ هَدَيْتَنَا وَهَبْ لَنَا مِن لَّدُنكَ رَحْمَةً إِنَّكَ أَنتَ الْوَهَّابُ ۝8
رَبَّنَا إِنَّكَ جَامِعُ النَّاسِ لِيَوْمٍ لَّا رَيْبَ فِيهِ إِنَّ اللَّهَ لَا يُخْلِفُ الْمِيعَادَ ۝9

ثمن

Suratu A'li Imrana

A madina aka saukar da ita Ayoyinta maitan (200)

Ina farawa dasunun Ubangiji Mai jiƙnan talikai a duniyagaba ɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

(TA ƘUNSHI KIRARI GA ALLAH MA-DAUKAKIN SARKI)

1. "A.L.M." (Allah ne yasan abinda yake nufi da wannan kalma) Allah babu abin bautawa da gaskiya sai Shi, "'ayayyan Sarkı mai tokare sammai da ƙassaida ƙarim ikonsa.
2. Ya sassaukar da Alƙur'ani a gareka a rarrabe (Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama) yana tareda gaskiya a cikin Labaransa, yana mai gasgalawa ga abinda ke gabansa (na daga littattafai) ya saukar da Attaura da Injlla (a mulmule).[1].
3. Tun gaban Alƙur'ani masu shiriyaga mutane kuma ya saukar da litattafai masu rabewa tsakanin gaskiya da ƙarya.
4. Waɗanda suka kafirtada ayoyin Allah (Alƙur'ani da waninsa) azaba mai tsanani ta tabbata a gare.su, Allah mabuwayi ne (a kan al'amarinsa, ba mai hana shi zartar da alƙawarinsa da narkwansa), ma'abocin azabane mai tsanani (ga wanda ya sabe shi, wacce ba wandazaiyi irinta).
5. Haƙiƙa Ubangiji ba abinda yake ɓuya a gareshi a cikin ƙasa ko a cikin sama, (saboda saninsa da abinda yakc atkuwa a cikin Alam. komai girmansa komai ƙanƙantarsa).
6. Shine wanda yake suranta ku a cikin mahaifa yadda yaga dama, (namiji ko mace, tari ko baki, ko wanin wannan.) ba abin bautawa da gaskiya sai shi. mabuwayi (a cikin mulki) gwani (a clkin aiki).

(MUHKAMU DA MUTASHABIHU WATAU AYOYI MASU MA' ANA A SARARI DA MARIKITA A CIKIN ALƘUR'ANI)

7. Shine wanda ya saukar da littafi a gareka, akwai ayoyi mabayyanan ma'anoni daga gareshi, sune asalin Alƙur'ani (wanda aka dogara kansa a cikin hukuncehukunce) da waɗansu marikitan ma'anomi (kamar far kon nin surori,) amma waɗanda karkata ga barin gaskiya take cikin zuciyarsu, to, suna bin abinda ya rikita daga gareshi, don neman fitina, da neman fassararsa, ba wanda yasan fassararsa kuwa sai Allah, matabbata a cikin sani kuwa suna cewa: "Mun bada gaskiya da marikicin ma'anan nan (cewa daga Allah yake (bamu san ma'anarsa ba) kowanne (daga mabayyanin ma'anar nan da marikicin ma'anan nan) daga Ubangijinmu yake," ba mai wa'azantuwa sai ma'abota hankula.
8. (Kuma suna cewa yayin da suka ga takadarun nan,) "ya Ubangijinmu' kadaka karkatar da zukatanmu (ga barin gaskiya da neman fassarar marikicin ma'ana wanda bai kamatada mu ba, tamfar daka karkatar da zukatan waɗancan takadaru) bayan ka shiryemu, bamu rahama daga gareka, haƙiƙa kai, kaine mai yawan baiwa.
9. "Ya Ubangijinmu! haƙiƙa kaine mai tara mutane a cikin rana wacce babu kokwanto a cikinta. (alƙiyama) haƙiƙa Ubangiji baya saɓa alƙawari".

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَن تُغۡنِيَ عَنۡهُمۡ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُهُم
مِّنَ ٱللَّهِ شَيۡـٔٗاۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمۡ وَقُودُ ٱلنَّارِ ١٠ كَدَأۡبِ ءَالِ فِرۡعَوۡنَ
وَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُ
بِذُنُوبِهِمۡۗ وَٱللَّهُ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ١١ قُل لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ
سَتُغۡلَبُونَ وَتُحۡشَرُونَ إِلَىٰ جَهَنَّمَۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمِهَادُ ١٢
قَدۡ كَانَ لَكُمۡ ءَايَةٞ فِي فِئَتَيۡنِ ٱلۡتَقَتَاۖ فِئَةٞ تُقَٰتِلُ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ
وَأُخۡرَىٰ كَافِرَةٞ يَرَوۡنَهُم مِّثۡلَيۡهِمۡ رَأۡيَ ٱلۡعَيۡنِۚ وَٱللَّهُ يُؤَيِّدُ
بِنَصۡرِهِۦ مَن يَشَآءُۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَعِبۡرَةٗ لِّأُوْلِي ٱلۡأَبۡصَٰرِ ١٣
زُيِّنَ لِلنَّاسِ حُبُّ ٱلشَّهَوَٰتِ مِنَ ٱلنِّسَآءِ وَٱلۡبَنِينَ
وَٱلۡقَنَٰطِيرِ ٱلۡمُقَنطَرَةِ مِنَ ٱلذَّهَبِ وَٱلۡفِضَّةِ وَٱلۡخَيۡلِ
ٱلۡمُسَوَّمَةِ وَٱلۡأَنۡعَٰمِ وَٱلۡحَرۡثِۗ ذَٰلِكَ مَتَٰعُ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۖ
وَٱللَّهُ عِندَهُۥ حُسۡنُ ٱلۡمَـَٔابِ ١٤ ۞ قُلۡ أَؤُنَبِّئُكُم بِخَيۡرٖ مِّن ذَٰلِكُمۡۖ حزب
لِلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ عِندَ رَبِّهِمۡ جَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا
ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا وَأَزۡوَٰجٞ مُّطَهَّرَةٞ وَرِضۡوَٰنٞ
مِّنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ بَصِيرُۢ بِٱلۡعِبَادِ ١٥

(RUDUWA DA YAWAN DUKIYA DA "YA"YA DA SA'BAMISALI BISA WANNAN)

10. Wađanda suka kafirta dukiyoyinsu da "ya" yansu baza suyi musu arnfanin komai daga azabar Allah ba, kuma wađancananka sunc gumaguman wuta.

11. (Al'adarsu) kamar al'adar Fir'uuna da mutancnsa, da wađanda suke gabansu (na daga al'umma kamar Aduda Siimudu, da basu gasgata ayoyinniu ba) Allah ya halakar dasu saboda zunubansu, Allah mai tsananin azaba ne.

(LABARI DA GAIBU)

12. (Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama!) Fadi ga wađanda suka kafirta (na Yahudawa) "da sannu za a rinjaye ku (a nan duniya da kisa da ribacewa da sanyajiziya, haka kuwa ya afku kamar yadda Allah ya bada labari) kuma za a tara ku a Lahira izuwajahannama, (ku shige ta,) tir! shimfida (ita')

(FIRGITA KAFIRAI DA RUNDUNAR MUSULMI A RANAR BADAR)

13. " Haƙiƙa izina ta kasance a gareku, a cikin jama'a guda biyu da suka gamu a ranar Badar don yaƙi, jama'a da take yaƙi saboda Allah, (Annabi Sallallahu alaihi wasallama da sahabbansa, su đari ukune da goma sha uku, suna da doki biyu da silke shida da takobi bakwai, yawaicinsu "yan sati ne, watau masu tafiya a ƙasa) da wata jama'ar kafira, kafirai suna ganm Musulmi sun ninka su biyu a yawa, (gasu ko su dubu ne) ganin ido, (Allah ya taimaki Musulmi tare da ƙarancinsu), Allah yana ƙarfafar wanda yaga dama (da talmakonsa,) haƙiƙa akwai izina a cikin wancananka (abin ambato) ga ma'abota basira".

(MUTUM DA SHA'AWAICE SHA'AWAICENSA NA DUNIYA)

14. An ƙawata wa mutane son sha'awaice sha'awaice, (Shaiđan ya ƙawata musu ita) na daga mataye da "ya" ya da dukiyoyi masu đinbin yawa na zinariya da azurfa, da dawaki kyawawa, da dabbobi, (rakuma) shanu, tumakai, da shuke - shuke, wanca-nanka (abin ambato) Jin dađin rayuwar duniya ne (ayi amfani dashi kađan sannan ya kare,) Allah kyakkyawar makomana ta tabbata gareshi, (Itace aljanna. Ya kamata a maida hankali ga abinda yake gun Allah, ba waninsa ba).

(ABINDA YAFI DUNIYA DA ABINDA YAKE CIKINTA)

15. Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama! fađi (ga mutanenka) shin bana baku labari ca mafifici daga wancananku (abin ambato ba watau sha'awaice -sha'awaice?) AlJannatai wacce ƙoramu suke kwarara ƙarƙashinta, tana ga Ubangijinsu (wađanda sukaji tsoron Allah,) masu dauwama a cikinta, akwai mataye ababan tsarkakewa (daga haila da waninta,) dayarda mai yawa duga Ubangiji. Allah rnasanine da bayinsa.

ٱلَّذِينَ يَقُولُونَ رَبَّنَآ إِنَّنَآ ءَامَنَّا فَٱغْفِرْ لَنَا ذُنُوبَنَا وَقِنَا
عَذَابَ ٱلنَّارِ ﴿16﴾ ٱلصَّٰبِرِينَ وَٱلصَّٰدِقِينَ وَٱلْقَٰنِتِينَ وَٱلْمُنفِقِينَ
وَٱلْمُسْتَغْفِرِينَ بِٱلْأَسْحَارِ ﴿17﴾ شَهِدَ ٱللَّهُ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ
وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَأُوْلُواْ ٱلْعِلْمِ قَآئِمَۢا بِٱلْقِسْطِ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ
ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿18﴾ إِنَّ ٱلدِّينَ عِندَ ٱللَّهِ ٱلْإِسْلَٰمُ
وَمَا ٱخْتَلَفَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلْكِتَٰبَ إِلَّا مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَهُمُ
ٱلْعِلْمُ بَغْيَۢا بَيْنَهُمْ وَمَن يَكْفُرْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ
سَرِيعُ ٱلْحِسَابِ ﴿19﴾ فَإِنْ حَآجُّوكَ فَقُلْ أَسْلَمْتُ وَجْهِيَ لِلَّهِ
وَمَنِ ٱتَّبَعَنِ وَقُل لِّلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْأُمِّيِّـۧنَ
ءَأَسْلَمْتُمْ فَإِنْ أَسْلَمُواْ فَقَدِ ٱهْتَدَواْ وَّإِن تَوَلَّوْاْ فَإِنَّمَا
عَلَيْكَ ٱلْبَلَٰغُ وَٱللَّهُ بَصِيرُۢ بِٱلْعِبَادِ ﴿20﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَكْفُرُونَ
بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَيَقْتُلُونَ ٱلنَّبِيٓـِٕينَ بِغَيْرِ حَقٍّ وَيَقْتُلُونَ
ٱلَّذِينَ يَأْمُرُونَ بِٱلْقِسْطِ مِنَ ٱلنَّاسِ فَبَشِّرْهُم
بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿21﴾ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ حَبِطَتْ أَعْمَٰلُهُمْ
فِي ٱلدُّنْيَا وَٱلْأٓخِرَةِ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ﴿22﴾

16. (Su ne) wađanda suke cewa: Ya Ubangijinmu! haƙiƙa, mu mun bada gaskiya (dakai da manzanninka,) sai ka gatarta mana zunubanmu, ka kiyashe mu azabar wuta.

17. (Su ne) masu haƙuri (a kan da'a da gudun saɓo,) masu gasgata (a cikiin imani,) masu biyayya (ga Allah,} masuyin alhairi (don Allah) masu neman gafarar Allah a lokatan Sahur (an keɓance Lokacin Sahur da ambato, saboda shi lakacin gatala ne da dađin bacci).

WAHADANIYAR ALLAH DA ADAL-CI DA MUSULUNCI NA HAƘIƘA)

18. Ubangiji ya bayyana ga halitta, (ta dalilan hankali da ayoyi, ta harshen manzanni,) hakika al'amari babu abin bautawa da guskiya sai Allah, Mala'iku sun shaidar da wannan da ma'abota ilimi, (Annabawa da mumina, u kudurinsu da harshensu,) makađaici da adalci. babu abin bautawa da gaskiya sai shi, inabuwayi (cikin mulkinsa,) gwani (a cikin aikinsa).

19. Haƙiƙar Addini (yardajje) nan ga Allah shine Dinil - Islami, wanda aka aiko manzanni dashi, aka gina shi a kan harsashin kađaita Allah) wađanda aka basu Littattafai (yahudu da Nasara) basu sassaba ba, (a cikin addini, (shine wađansu suka kađaita shi wađansu suka kafirta dashi) sai bayan sanin Tauhidi yazo musu, don lawaye na kafiran nan a tsakaninsu. duka wanda ya kafirtada ayoyin Allah, haƙiƙa, Ubangiji mai gaggawar sakamako ne (a gareshi).

(MUSULUNCI NA HAƘIƘA)

20. Idan kafirai sukayi husuma dakai (ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama, a cikin addini.) to,. cene (dasu,) "Na miƙa zatina ga Allah, na jawu gareshi gabađaya ni da wanda yabini," (an keɓanci fuska da ambato saboda daukakarta a kan sauran gaɓuɓuwa, ai na miƙa fuskata balle sauran gaɓuɓuwana) kuma ka fađa ga wađanda aka basu littafi (Yahudu da Nasara,) Wal ummiyyina - ai jahilai wato mushirikan Larabawa,) "Ku Musulunta" to, in suka Mlisulunta, to, haƙiƙa sun shiriya (daga ɓata) in ko suƙa bada baya (ga barin Musulunci,) to, iyar da aike ne kawai a kanka, Allah masanine da bayi. (Wannan gaban umarni dayaƙi ne).

(SAKAMAKON KISAN ANNABAWA DA MALAMAI)

21. Wađanda suke kafirtada ayoyin Allah, suke kashe Annabawa ba gaira badalili- suke kashe wađanda suke umarni da adalci na daga mutane, (sune Yahu-dawa, sun kashe Annabi arba'in da uku, da malamai đari da saba'in wađanda sukayi musu gargađi a kan wannan mugun aiki a rana đaya) to, yi musu albishir da azaba mai rađađi.

22. Wađancananka sune wađanda ayyukansu suka lalace, (kamar sadaka da sada zumuntada sauransu,) a duniya da Lahira, (basu da amfani a Lahira, don ba Musulunci garesu,) basu da mai hana musu azaba.

ثمن

أَلَمْ تَرَ إِلَى الَّذِينَ أُوتُواْ نَصِيباً مِّنَ الْكِتَٰبِ يُدْعَوْنَ
إِلَىٰ كِتَٰبِ اللَّهِ لِيَحْكُمَ بَيْنَهُمْ ثُمَّ يَتَوَلَّىٰ فَرِيقٌ مِّنْهُمْ
وَهُم مُّعْرِضُونَ (23) ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ قَالُواْ لَن تَمَسَّنَا النَّارُ إِلَّا
أَيَّاماً مَّعْدُودَٰتٍ وَغَرَّهُمْ فِي دِينِهِم مَّا كَانُواْ يَفْتَرُونَ (24)
فَكَيْفَ إِذَا جَمَعْنَٰهُمْ لِيَوْمٍ لَّا رَيْبَ فِيهِ وَوُفِّيَتْ كُلُّ نَفْسٍ مَّا كَسَبَتْ
وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ (25) * قُلِ اللَّهُمَّ مَٰلِكَ الْمُلْكِ تُؤْتِي الْمُلْكَ
مَن تَشَآءُ وَتَنزِعُ الْمُلْكَ مِمَّن تَشَآءُ وَتُعِزُّ مَن تَشَآءُ وَتُذِلُّ
مَن تَشَآءُ بِيَدِكَ الْخَيْرُ إِنَّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ (26) تُولِجُ
الَّيْلَ فِي النَّهَارِ وَتُولِجُ النَّهَارَ فِي الَّيْلِ وَتُخْرِجُ الْحَيَّ مِنَ الْمَيِّتِ
وَتُخْرِجُ الْمَيِّتَ مِنَ الْحَيِّ وَتَرْزُقُ مَن تَشَآءُ بِغَيْرِ حِسَابٍ (27)
لَّا يَتَّخِذِ الْمُؤْمِنُونَ الْكَٰفِرِينَ أَوْلِيَآءَ مِن دُونِ الْمُؤْمِنِينَ وَمَن يَفْعَلْ
ذَٰلِكَ فَلَيْسَ مِنَ اللَّهِ فِي شَيْءٍ إِلَّا أَن تَتَّقُواْ مِنْهُمْ تُقَٰةً
وَيُحَذِّرُكُمُ اللَّهُ نَفْسَهُ وَإِلَى اللَّهِ الْمَصِيرُ (28) قُلْ إِن تُخْفُواْ
مَا فِي صُدُورِكُمْ أَوْ تُبْدُوهُ يَعْلَمْهُ اللَّهُ وَيَعْلَمُ مَا فِي السَّمَٰوَٰتِ
وَمَا فِي الْأَرْضِ وَاللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ (29)

(BIJIREWA GA BARIN HUKUNCIN ALLAH TAREDA RUDIN KAI)

23. Yi duba mana izuwa wađanda aka basu rabo na Attaura, ana kiran su izuwa littafin Allah donya yo hukunci a tsakaninhu, sannan wađansu jama'a daga cikinsu suna bada baya alhali su sunamasu bijirewa.

24. Wancananka (Juya baya da bijirewa) saboda haƙiƙa, su sunce "Wuta bazata taɓa mu ba sai kwanika ababan ƙirgawa" (kwana arba'in muddar da iyayensu sukayi bautar Dan maraki,) abinda suke ƙirƙira ya ruɓe su a cikin addininsu, (shine fađinsu "Wuta bazata taɓamu ba").

25. Ka ga halinsu idan muka tara su a cikin rana wacce babu kokonto a cikinta, aka cikawa kowace kai abin data aikata (na hairi ko sharri,) su mutane ɓaza a zalince su ba, (da tauye hasana[1] ko ƙari cikin sayyi'a)[2]

(ƘASAITAR ALLAH a GIRMANSA DA IKONSA)

26. (Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama! fađi; "Ya Ubangiji! mana llakin sarauta, kana bada sarauta ga wandaka ga dama (daga halittarka,) kana karɓe sa" rauta daga wandaka ga dama, kana buwayanta wandaka ga dama, (da nađa shi) kana ƙaskanta wandaka ga dama (da tuɓe shi,) alhairi (da sharri,) yana hannunka, haƙiƙa kai mai iko ne bisa komai.

27. "Kana shigar da dare a cikin rana, kana shigar da rana a cikin dare, (kowane đayansu, ya karu da abinda đayansu ya tawaya dashi,) kana fitar da rayayye daga matacce, (kamar mutun daga maniyyi. tsuntsu daga kwai,) kana fitar da matacce daga mai rai, (kamar maniyyi da kwai,) kana azurta wandaka ga dama, (arziki mayalwaci) bada lissafi ba".

(MA'AMALAR MUSULMI DA KAFIRI DA TSORATARWA DAGA RANAR LAHIRA)

28. Kada niuminai su daukaki kafirai (watau kadasu rungume su baka da hanci) abokan mu'amala, ba muminai ba, wanda ya aikata wannan, baya cikin komai (na daga addinin Allah) to. sai ko m kun yi hatlara matukar hattara daga garesu. (saboda raunin musulunci, da bukatuwarku izuwa ma'amula dasu, to, ya halatta gareku kuyi ma'amala dasu. alallarurati gwargwadon bukata ba tareda daukaka ba, watau rungumarsu, baka da hanci). Allah yana razanar daku ,kansa, izuwa Allah makomarku.

29. Cene (dasu) "In kun ɓoye abinda yake cikin ƙirajenku. (na daukaka,) ko kuka bayyana shi Allah yasan shi, Allah yana sanc da abinda yake cikin saminai da abinda yake cikin ƙassai, Allah mai iko ne bisa komai (da yake nufinsa)".

1) Aikin Kiri
2) Mum Munan Aiki.

يَوْمَ تَجِدُ كُلُّ نَفْسٍ مَّا عَمِلَتْ مِنْ خَيْرٍ مُّحْضَرًا وَمَا عَمِلَتْ مِن
سُوٓءٍ تَوَدُّ لَوْ أَنَّ بَيْنَهَا وَبَيْنَهُۥٓ أَمَدًۢا بَعِيدًا وَيُحَذِّرُكُمُ اللَّهُ نَفْسَهُۥ
وَاللَّهُ رَءُوفٌۢ بِالْعِبَادِ ﴿30﴾ قُلْ إِن كُنتُمْ تُحِبُّونَ اللَّهَ فَاتَّبِعُونِي
يُحْبِبْكُمُ اللَّهُ وَيَغْفِرْ لَكُمْ ذُنُوبَكُمْ وَاللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿31﴾
قُلْ أَطِيعُوا اللَّهَ وَالرَّسُولَ فَإِن تَوَلَّوْا فَإِنَّ اللَّهَ لَا يُحِبُّ
الْكَٰفِرِينَ ﴿32﴾ * إِنَّ اللَّهَ اصْطَفَىٰٓ ءَادَمَ وَنُوحًا وَءَالَ إِبْرَٰهِيمَ ربع
وَءَالَ عِمْرَٰنَ عَلَى الْعَٰلَمِينَ ﴿33﴾ ذُرِّيَّةًۢ بَعْضُهَا مِنۢ بَعْضٍ
وَاللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿34﴾ إِذْ قَالَتِ امْرَأَتُ عِمْرَٰنَ رَبِّ إِنِّي نَذَرْتُ
لَكَ مَا فِي بَطْنِي مُحَرَّرًا فَتَقَبَّلْ مِنِّيٓ إِنَّكَ أَنتَ السَّمِيعُ الْعَلِيمُ ﴿35﴾
فَلَمَّا وَضَعَتْهَا قَالَتْ رَبِّ إِنِّي وَضَعْتُهَآ أُنثَىٰ وَاللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا وَضَعَتْ
وَلَيْسَ الذَّكَرُ كَالْأُنثَىٰ وَإِنِّي سَمَّيْتُهَا مَرْيَمَ وَإِنِّيٓ أُعِيذُهَا بِكَ
وَذُرِّيَّتَهَا مِنَ الشَّيْطَٰنِ الرَّجِيمِ ﴿36﴾ فَتَقَبَّلَهَا رَبُّهَا بِقَبُولٍ حَسَنٍ
وَأَنۢبَتَهَا نَبَاتًا حَسَنًا وَكَفَّلَهَا زَكَرِيَّآءُ كُلَّمَا دَخَلَ عَلَيْهَا
زَكَرِيَّآءُ الْمِحْرَابَ وَجَدَ عِندَهَا رِزْقًا قَالَ يَٰمَرْيَمُ أَنَّىٰ لَكِ هَٰذَا
قَالَتْ هُوَ مِنْ عِندِ اللَّهِ إِنَّ اللَّهَ يَرْزُقُ مَن يَشَآءُ بِغَيْرِ حِسَابٍ ﴿37﴾

30. (Ka ainbata musu); "Ranar da kuwace kai take samun abindata aikata na hairi abin halartarwa, abindata aikata mummuna kuwa, tana burin da hakika akwai fage mai nisa, tsakanin tada tsakaninsa, Allah yana firgitar daku ,kansa, Allah mai tsan-anin jinƙai ne ga bayi.

MAHABBATULLAH! LA' AƘAUNAR ALLAH SAITAKE DA .BIN MA' AIKINSA SALLAL LAHU ALAIHI WA SALLAMA

31. (Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama! Cene (da waɗanda sukace Barna bautar gumaka sai don ƙaunar Allah, kuma don neman su kusantamu gareshi,) "In kun kasance kuna son Allah, to, kubini, Allah sai yaso ku, ya gafarta Muku zunubanku, ALLAH mai yawan gafara ne (ga wanda yabi ru. zai gafarta masa abinda ya wuce gaban wannan,) mai yawan jinƙai (dashi)".

32. Cene (dasu,) "Kubi Allah da manzonsa (cikin abinda yake umarninku dashi na bautar Allah,) "to, in sun bada baya (ga barin ɗa'a,) to, haƙiƙa Allah ha yason kafirai.

(FIFIKON ANNANBAWA DA ZURIY-ARSU A KAN HALITTA)

33. Haƙiƙa Ubangiji ya zaɓi Annabi Adamu da Annabi Nuhu da "ya"yan Annabi Ibmhimu da "ya"yan Imranu a bisa lalikai (na zamaninsu).

34. Zuri'a ba'alinsu daga ba'ali. Allah mai yawan ji ne mai yawan sani.

(HIMMAR MASANA ALLAH A CIKIN SHA'ANIN ALLAH)

35. (Ka ambata) zamanin da matar Imranu (Itace Hannatu yayin data tsufa ta beganci haihuwa, ta roƙi Allah, tayi hasashe da samun ciki,) "Ya Ubangijina! haƙiƙa m nayi alwashin abinda yake cikin cikina ya zan abin "yantawa, ga hidimarka kawai, don neman yardarka, sai ka karɓa daga gare ni, haƙiƙa kai kaine mai ji, (kaine maji roƙo,) Masani (da niyyoyi). Imranu ya mutu yabar tada ciki)".

36. Yayin data haife ta, tamata, (ita ko yaro take so da, dan shine zai fi dacewa da hidimar Baitil Maƙdisi) tace, (tana mai hanzari,) "Ya Ubangijina, Haƙiƙa ni nahaifeta ta matada ma Allah yasan abindata haifa," namiji (wandana nema) bai kasance kamar mace da aka bani ba, (saboda ita mace bata kyautuwa da hidimar Dakin Allah mai tsarki don raunintada zamanta al'aura da abinda yake samuni-a na haila da makamancinsa). Ni haƙiƙa na ambace ta Maryamu, kuma ni, ina neman mata tsari gun ka itada zuriyarta daga shaiɗan abin la'anta,"(Acikin Haldisi babu wani abin haihuwa daza a haife shi face shaiɗan ya zungure shi yayin daza a haifar ya faɗo yana mai kururuwa, sai Maryamu da danta, inji Bukhari da Muslim).

KARAMATUL - AULIYA I WATAU: KARAMOMIN WALIYAN ALLAH

37. Sai Ubangijinta ya karɓe ta (Maryamu) daga uwartada karɓa kyakkyawa. (ya raya ta, watau shine) ya tsirar da ita tsi-rarwa kyakkyawa, (tana dabuwa a rana daya kamar yadda yaro yake daɗuwa a shekara). Annabi Zakariya'u ya raine ta, koyaushe Annabi zakariyau ya shiga Mihrabi a gare ta (watau gurin tsaiwar liman) ya sami arziki nan gare ta, sai yace: "Ya Maryamu daga ina ki ka sami wannan?" Saitace: (alhali tana "yar ƙanƙanuwa a cikin gunya) "Shi daga Allah yake (yana kawo mini shi daga Aljanna, ubangiji yana azurta wanda yaga dama (arziki mayalwaci) bada ƙidaya ba".

هُنَالِكَ دَعَا زَكَرِيَّآءُ رَبَّهُۥ قَالَ رَبِّ هَبْ لِے مِن لَّدُنكَ ذُرِّيَّةً
طَيِّبَةً اِنَّكَ سَمِيعُ اُ۬لدُّعَآءِ ﴿38﴾ فَنَادَتْهُ اُ۬لْمَلَٰٓئِكَةُ وَهْوَ قَآئِمٞ
يُصَلِّے فِے اِ۬لْمِحْرَابِ أَنَّ اَ۬للَّهَ يُبَشِّرُكَ بِيَحْيَىٰ مُصَدِّقاَۢ بِكَلِمَةٖ
مِّنَ اَ۬للَّهِ وَسَيِّداٗ وَحَصُوراٗ وَنَبِيٓـٔاٗ مِّنَ اَ۬لصَّٰلِحِينَ ﴿39﴾
قَالَ رَبِّ أَنَّىٰ يَكُونُ لِے غُلَٰمٞ وَقَدْ بَلَغَنِيَ اَ۬لْكِبَرُ
وَامْرَأَتِے عَاقِرٞ قَالَ كَذَٰلِكَ اَ۬للَّهُ يَفْعَلُ مَا يَشَآءُ ﴿40﴾ قَالَ رَبِّ
اِجْعَل لِّيَ ءَايَةٗ قَالَ ءَايَتُكَ أَلَّا تُكَلِّمَ اَ۬لنَّاسَ ثَلَٰثَةَ أَيَّامٍ
اِلَّا رَمْزاٗ وَاذْكُر رَّبَّكَ كَثِيراٗ وَسَبِّحْ بِالْعَشِيِّ وَالْإِبْكَٰرِ ﴿41﴾
* وَإِذْ قَالَتِ اِ۬لْمَلَٰٓئِكَةُ يَٰمَرْيَمُ إِنَّ اَ۬للَّهَ اَ۪صْطَفَىٰكِ وَطَهَّرَكِ
وَاصْطَفَىٰكِ عَلَىٰ نِسَآءِ اِ۬لْعَٰلَمِينَ ﴿42﴾ يَٰمَرْيَمُ اُ۪قْنُتِے
لِرَبِّكِ وَاسْجُدِے وَارْكَعِے مَعَ اَ۬لرَّٰكِعِينَ ﴿43﴾ ذَٰلِكَ مِنْ أَنۢبَآءِ
اِ۬لْغَيْبِ نُوحِيهِ إِلَيْكَ وَمَا كُنتَ لَدَيْهِمْ إِذْ يُلْقُونَ أَقْلَٰمَهُمْ
أَيُّهُمْ يَكْفُلُ مَرْيَمَ وَمَا كُنتَ لَدَيْهِمْ إِذْ يَخْتَصِمُونَ ﴿44﴾ إِذْ قَالَتِ
اِ۬لْمَلَٰٓئِكَةُ يَٰمَرْيَمُ إِنَّ اَ۬للَّهَ يُبَشِّرُكِ بِكَلِمَةٖ مِّنْهُ اُ۪سْمُهُ اُ۬لْمَسِيحُ
عِيسَى اَ۪بْنُ مَرْيَمَ وَجِيهاٗ فِے اِ۬لدُّنْيَا وَالْأٓخِرَةِ وَمِنَ اَ۬لْمُقَرَّبِينَ ﴿45﴾

ثمن

(KA,DA KABAR DAMA TA WUCL K.A" WADDA ƘISSAR ANNABI ZAKA-RIYA'LJ DA ANNABI YAHAYA TA ƘUNSA TSIRAN ALLAH DA AMINCIN ALLAH YA TABBATA GARESU)

38. Cananka ne (yayin da Zakariya'u yaga cewa mai iko bisa zuwa da abu, ba a lokacinsa ba, mai iko ne bisa bashi da tare ɗa tsufansa, da ƙarewar "ya"yansa) ya roƙi Ubangijin.sa (a tsakar dare cikin Mihrabinsa) yace "Ubangijina! bani zuriya tsartsarka daga gareka, (ɗa managarci,) haƙiƙa kai mai jin roƙo ne".

39. Sai Mala'ika (Jibrilu) ya kirawo shi (bayan shekara arba'In daga yin addu'a) yana tsaye, a cikin masallaci. " haƙiƙa Ubangiji yanayi maka albishir da Annabi Yahaya mai gasgatawa da kalma daga Allah, Annabi (isa Alaihissalam, cewa shi Ruhul -Lahi ne an ambace shi da "kalma" saboda an halicce shi da kalmar KUN) kuma shugaba marar sha'awar mata, Annabi daga cikin annabawa managarta". (A cikin Hadisi cewa shi bai taɓa aikata kuskure ba, bai taɓa ruwaita shi a ransa ba).

40. Yace "Ubangijina! yaya dazai samu gare ni? Haƙiƙa girma ya riske ni (shekara ta ɗari da ashirin) matala kuma bakarara ce;(watau bata taɓa haihuwa ba shekarar ta casa'in da takwas) yace: "Al'amarin haka yake (Allah zai halicci ɗa daga gare ku,) Allah yana aikata abinda yaga dama" (ba abinda yake gaji dashi, an kimsa masa wannan tambaya waddata kunshi ƙudira mai girma don a bashi amsa da.

ALLAHU YAFALU MA YA SHA'U).

41. yace, (saboda gauƙassa [1] izuwa abinda akayi masa albishir dashi); yace "Ubangijina! sanya min aiama abisa samun wannan da "Alamar ka (a kansa) ka ƙasa zance da mutane sai zikirullahi, kwana uku (da dararanta,) sai ko ishara, ambaci Ubangijinka ambato mai yawa, kayi sallah dayamma da safiya".

(MANA MARYAMU DA DARAJARTA)

42. (Ka ambata) zamanin da Mala'ika (Jibrilu) yace "ya Maryamu haƙiƙa Ubangiji ya zabe ki, ya tsarkake ki (daga saduwa da maza,) yafifita ki a kan matan talikai (na zamaninki).

43. "Ya Maryamu! yi biyayya ga Ubangijinki, dungura goshinki kiyi sallah tareda masallata".

44. Wancananka (abin ambato, sha'anin Annabi Zakariya'u da Nana Maryamu) yuna daga labaran gaibu, muke aiko shi izuwa gareka, *ya Annabi Saallaahu alaihi wasailama) baka kasance garesu ba, zamanin dasuke jela alƙalimansu (cikin ruwa suna yin ƙuri'a donya buyyana gaie-su) wannenan.su zai raini Maryamu' baka kasance garesu bazamanin dasuke husuma (,a cikin rainanta, balle kasan wannan har ka bada Labari dashi, kasan shine daga Wahayi).

WANI ABU DAGA DARA JOJIN ANNABI ISA ALAIHISSALAMU WANDA ƘISSAR TA ƘUNSA

45. (Ka amhata) zamanin da Mala'ika (Jibrilu) yace "Ya Maryamu'. haƙiƙa Allah yanayi miki albishir da ɗa daga gareshi sunansa abin sawa albarka a cikin duk abinda ya taɓa, Isa ɗan Maryamu (an dangana shi izuwa gareta saboda an same slii nc bada uba ba,) mai altarma da Annabci a duniya (mai alfarma) a Lahira (da ceto da daraja maɗaukakiya,) kuma yana daga makusanta.

1). Wato isanamn bukatuwarsa.

وَيُكَلِّمُ ٱلنَّاسَ فِي ٱلۡمَهۡدِ وَكَهۡلٗا وَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿46﴾ قَالَتۡ
رَبِّ أَنَّىٰ يَكُونُ لِي وَلَدٞ وَلَمۡ يَمۡسَسۡنِي بَشَرٞۖ قَالَ كَذَٰلِكِ
ٱللَّهُ يَخۡلُقُ مَا يَشَآءُۚ إِذَا قَضَىٰٓ أَمۡرٗا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ﴿47﴾
وَيُعَلِّمُهُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ وَٱلتَّوۡرَىٰةَ وَٱلۡإِنجِيلَ
وَرَسُولًا إِلَىٰ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ أَنِّي قَدۡ جِئۡتُكُم بِـَٔايَةٖ مِّن رَّبِّكُمۡ
أَنِّيٓ أَخۡلُقُ لَكُم مِّنَ ٱلطِّينِ كَهَيۡـَٔةِ ٱلطَّيۡرِ فَأَنفُخُ فِيهِ فَيَكُونُ
طَيۡرَۢا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۖ وَأُبۡرِئُ ٱلۡأَكۡمَهَ وَٱلۡأَبۡرَصَ وَأُحۡيِ
ٱلۡمَوۡتَىٰ بِإِذۡنِ ٱللَّهِۖ وَأُنَبِّئُكُم بِمَا تَأۡكُلُونَ
وَمَا تَدَّخِرُونَ فِي بُيُوتِكُمۡۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ لَّكُمۡ
إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ﴿48﴾ وَمُصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيَّ مِنَ ٱلتَّوۡرَىٰةِ
وَلِأُحِلَّ لَكُم بَعۡضَ ٱلَّذِي حُرِّمَ عَلَيۡكُمۡۚ وَجِئۡتُكُم بِـَٔايَةٖ
مِّن رَّبِّكُمۡ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿49﴾ إِنَّ ٱللَّهَ رَبِّي وَرَبُّكُمۡ
فَٱعۡبُدُوهُۚ هَٰذَا صِرَٰطٞ مُّسۡتَقِيمٞ ﴿50﴾ * فَلَمَّآ أَحَسَّ
عِيسَىٰ مِنۡهُمُ ٱلۡكُفۡرَ قَالَ مَنۡ أَنصَارِيٓ إِلَى ٱللَّهِۖ قَالَ ٱلۡحَوَارِيُّونَ
نَحۡنُ أَنصَارُ ٱللَّهِ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَٱشۡهَدۡ بِأَنَّا مُسۡلِمُونَ ﴿51﴾

ربع

46. "Yana zance da mutane a cikin gunya (ai yana jariri,) kuma dayana gwarzo[1] yana cikin managarta".

47. Tace: "Ubangijina ƙaƙa ɗa zai samu gare ni, alhali wani bil -Adama bai sadu dani ba, (da aure ko wanin.sa?) Yace:"Al'amarin haka yake (halittar da daga gareki bada uba ba, hikimar tambaya kamar na farko ne) Allah yana halittar abinda yake nufi, idan yanufi al'amari, (yanufi samar dashi,) yana cewa dashiya samune kawai! to, shi abm nan saiya samu.

48"Yasanar dashi mbutu da hikima da Attaura da Linjila. kuma (Ya sanyashi) manzo izuwa Bani'isra'ila, (a cikin ƙuruciya," sai Jibrilu yayi busa a cikin aljihun rigarta, saitayi ciki. Cikakkcn bayani yana tafe a cikin Suratu Maryam, yace): " Haƙiƙa ni nazo mukuda alama bisa gaskiyata daga Ubangijinku, shine haƙiƙa ni ina suranta muku, sura ta tsuntsu daga yunɓu, in busa a cikin surar nan saiya zama tsuntsu da izmin Allah, (ya gina musu Jemage. saboda yafi tsuntsaye cikar halitta, yana tashi, mutane suna kallonsa, idan ya faku ga barin ganinsu saiya fadl matacce,) ina warkar da makahon da aka haitada makantada kuturu, (an keɓance su da ambato saboda su , cutuka ne masu wahalarwa, an aiko shi a cikin zamanin gwanintar tsibbu, ya warkar da mutum dubu hamsin a rana ɗaya da addu'a bisa sharaɗin imani) ina raya maiattu da izinin Allah, (ya raya abokinsa Azaru da ɗan tsohuwa, da ɗan wani kwastan, aka haifa masa "ya"yaye suka rayu suka hayayyafa da Samu dan Nuhu amma ya mutu a Lokacin,) ina baku Labari da abindaku ,ke ci da abindaku ,ke ɓoye wa a cikin dakunanku, (yakan gaya wa mutum abinda yaci da abindazai ci nan gaba) hakika a cikin wancananka Lallai akwai aya a gareku in kun kasance muminai.

49. ("Nazo muku) mai gasgatawa da abinda yake gabana na Attaura, kuma don in halarta a gareku sashin abinda aka haramta a gareku (a cikmta, ya halatta musu kifi da tsuntsu waɗanda basu da ƙaya), nazo mukuda aya daga Ubangijinku. sai kuji tsoron Allah kubini (cikin abinda nakc umarninku dashi na kaɗaita Allh ɗa da'a gareshi).

50. " Haƙiƙa Allah ne Ubangijina, Ubangijinku (watau ni badan Allah ne ba, ba Allah ba ne) to, ku bauta masa, wannan (abinda nake umarninku dashi) shine hanya madaidaiciya, (suka ƙaryata shi)".

(CI GABA: KTSSAR ANNABI ISA ALAIHISSAI.AM UA HAWARIYY-AWA SAHABBANSA YADDAR ALLAH TA TABBATA A GARESU

51. Yayin da Annabi Isa ya tabbatar da kafirci a garesu, (suka nufi kashe shi,) sai yace "Su waye mataimakana ina mai tafiya izuwa Allah (don in taimaki addininsa?)" Hawariyyawa (watau keɓantattun mutanensa, guda goma sha biyu) sukace "Mune mataimakan Allah, mun bada gaskiya da Allah, (Ya Annabi Isa) shaida da cewa mu, Lallai musulman haƙiƙa ne.

1) gwarzo : watan zamanin da zaya sakko daga -ianii Karshcn duniva

رَبَّنَا ءَامَنَّا بِمَا أَنزَلْتَ وَاتَّبَعْنَا الرَّسُولَ فَاكْتُبْنَا مَعَ الشَّٰهِدِينَ ۝52
وَمَكَرُواْ وَمَكَرَ اللَّهُ وَاللَّهُ خَيْرُ الْمَٰكِرِينَ ۝53 إِذْ قَالَ
اللَّهُ يَٰعِيسَىٰ إِنِّي مُتَوَفِّيكَ وَرَافِعُكَ إِلَيَّ وَمُطَهِّرُكَ مِنَ الَّذِينَ
كَفَرُواْ وَجَاعِلُ الَّذِينَ اتَّبَعُوكَ فَوْقَ الَّذِينَ كَفَرُواْ إِلَىٰ يَوْمِ
الْقِيَٰمَةِ ثُمَّ إِلَيَّ مَرْجِعُكُمْ فَأَحْكُمُ بَيْنَكُمْ فِيمَا كُنتُمْ
فِيهِ تَخْتَلِفُونَ ۝54 فَأَمَّا الَّذِينَ كَفَرُواْ فَأُعَذِّبُهُمْ عَذَابًا
شَدِيدًا فِي الدُّنْيَا وَالْأَخِرَةِ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ۝55
وَأَمَّا الَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ الصَّٰلِحَٰتِ فَنُوَفِّيهِمُ أُجُورَهُمْ
وَاللَّهُ لَا يُحِبُّ الظَّٰلِمِينَ ۝56 ذَٰلِكَ نَتْلُوهُ عَلَيْكَ
مِنَ الْأَيَٰتِ وَالذِّكْرِ الْحَكِيمِ ۝57 إِنَّ مَثَلَ عِيسَىٰ
عِندَ اللَّهِ كَمَثَلِ ءَادَمَ خَلَقَهُۥ مِن تُرَابٍ ثُمَّ قَالَ لَهُۥ كُن
فَيَكُونُ ۝58 الْحَقُّ مِن رَّبِّكَ فَلَا تَكُن مِّنَ الْمُمْتَرِينَ ۝59 فَمَنْ
حَاجَّكَ فِيهِ مِنۢ بَعْدِ مَا جَاءَكَ مِنَ الْعِلْمِ فَقُلْ تَعَالَوْاْ نَدْعُ
أَبْنَاءَنَا وَأَبْنَاءَكُمْ وَنِسَاءَنَا وَنِسَاءَكُمْ وَأَنفُسَنَا وَأَنفُسَكُمْ
ثُمَّ نَبْتَهِلْ فَنَجْعَل لَّعْنَتَ اللَّهِ عَلَى الْكَٰذِبِينَ ۝60

52. "ya Ubangijinmu' mun bada gaskiya da abinda ka saukar (na Injila) mun bi manzonka (Annabi Isa,) rubutamu tareda masu shaidawa (gareka da ɗayantaka, kuma ga manzonka da gasgatawa).

53. kafiran Bani'isra'ila sukayi makirci (da Annabi Isa, suka shirya wandazaiyi masa kisan gila,) Allah ya shirya musu sakamakon makircin, (shine sanya ka-mannin Annabi Isa ga wannan da suka shirya yayi kisan gila, suka kashe shi, watau ƙaiƙayi yakoma kan masheƙiYake nan Allah ya ɗauke shi izuwa sama,) Allah .shine ya fi makirai; sakamakon makirci.

54. (Ambaci) zamanin da Allah yace "Ya Isa! Ni mai karɓar ka ne, mai ɗaukaka ka ne izuwa fadata, (daga duniyaba tareda mutuwa ba,) ni mai nisanta ka ne daga waɗanda suka kafirta, mai sanya waɗanda sukabika (na Musulmi da Nasara) ne birbishin waɗanda suka kafirtadakai (sune Yahudu, da ƙarfin hujja da kansakali,) izuwa ranar Alƙiyama, sannan makomarku ta tabbata izuwa gare ni , in yi hukunci tsakaninku cikin abinda kuka kasance kuna sassabawa a cikinsa (na al'amarin addini. Allah ya fada masa haka ne saboda albi.shir da tsira daga sharrin Yahudawa).

55. "To, amma waɗanda suka kafirta zan yi musu azaba, azaba mai tsanani a duniya (da kisa da ribacewa da Jiziya) haka a Lahira (da wuta) basu da masu hana musu azaba.

56. "Amma waɗanda suka bada gaskiYakuwa, sukayi aiki nagari, to, zan cika musu sakamakonsu, Allah ba yason azzalimai.(Acikin Hadisi: Allah ya aiko girgije izuwa gareshiya dau ke shi sai uwarsa ta rataya dashi ta fashe da kuka yace da ita "Ma haɗu a ranar Lahira,"; a Daren Lailatulƙadri akayi wannan a Baitul-maƙdisi yana ɗan shekara talatin da uku, mahaifiyarsa ta rasu bayan shekara shida da ɗauke shi, Buhari da Muslim sunce "Zal sauka dab da Alƙiyama, zaiyi hukunci da shari'ar Annabinmu, zai kashe Dujal da Alhinzir, zai karya kere zai ajiyejiziya).

57. "Wannan (abin ambato na al'amarin Annabi Isa Alaihissalamu) muna karanta shi a gareka (ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama) na daga ayoyi da ambato abin ingantawa (Alƙur'ani)".

(RADDI BISA ALLANTAKAR ISA ALAIHISSALAMU DA ƘISSAR TSINAKAYYA)

58. Haƙiƙa misalin sha'anin Annabi Isa, (na mana ki nan ga Allah,) kamar sha'anin Annabi Adamu ne, (tsiran Allah ya tabbata a garesu, ya halicce shi bada uba ba, an kamanta mai ban mana ki da mafi ban mana ki don yafi yankan hanzari ga mai jayayya yayi tasiri azuci) Allah ya halicci gan gar jikinsa daga turɓaya, sannan yace dashi:"Zama (mutum)": Yakuwa zama (mutum ɗin, hakana Annabi Isa yace dashi samu bada uba ba yako samu).

59. (Al'amarin Annabi Isa) gaskiya ne daga Ubangijinka, kadaka zamo daga cikin masu kokonto (a cikinsa).

60. To, duk wanda .yayi jayayya dakai (daga Nasara) a cikin sha'anin Annabi Isa, bayan abinda yazo maka na sani (da al'amarnsa,) to, cene (dasu):"Kuzo mu kira "ya"yanmu da "ya"yanku, da matanmu da matanku, da kawukanmu da ƙawukanku, mu hadu sannan mu ƙanƙan dakai a cikin addu'a, mu sanya tsinewar Allah bisa maƙaryata, (ai muce Allah ya tsinewa maƙaryaci a cikin sha'anin Annabi Isa)".

ثمن

إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ الْقَصَصُ الْحَقُّ وَمَا مِنْ إِلَٰهٍ إِلَّا اللَّهُ وَإِنَّ اللَّهَ
لَهُوَ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ ﴿61﴾ فَإِن تَوَلَّوْا فَإِنَّ اللَّهَ عَلِيمٌ بِالْمُفْسِدِينَ ﴿62﴾
* قُلْ يَا أَهْلَ الْكِتَابِ تَعَالَوْا إِلَىٰ كَلِمَةٍ سَوَاءٍ بَيْنَنَا
وَبَيْنَكُمُ أَلَّا نَعْبُدَ إِلَّا اللَّهَ وَلَا نُشْرِكَ بِهِ شَيْئًا وَلَا يَتَّخِذَ
بَعْضُنَا بَعْضًا أَرْبَابًا مِّن دُونِ اللَّهِ فَإِن تَوَلَّوْا
فَقُولُوا اشْهَدُوا بِأَنَّا مُسْلِمُونَ ﴿63﴾ يَا أَهْلَ الْكِتَابِ لِمَ تُحَاجُّونَ
فِي إِبْرَاهِيمَ وَمَا أُنزِلَتِ التَّوْرَاةُ وَالْإِنجِيلُ إِلَّا مِنۢ بَعْدِهِ
أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿64﴾ هَا أَنتُمْ هَٰؤُلَاءِ حَاجَجْتُمْ فِيمَا لَكُم بِهِ عِلْمٌ
فَلِمَ تُحَاجُّونَ فِيمَا لَيْسَ لَكُم بِهِ عِلْمٌ وَاللَّهُ يَعْلَمُ وَأَنتُمْ
لَا تَعْلَمُونَ ﴿65﴾ مَا كَانَ إِبْرَاهِيمُ يَهُودِيًّا وَلَا نَصْرَانِيًّا
وَلَٰكِن كَانَ حَنِيفًا مُّسْلِمًا وَمَا كَانَ مِنَ الْمُشْرِكِينَ ﴿66﴾ إِنَّ أَوْلَى
النَّاسِ بِإِبْرَاهِيمَ لَلَّذِينَ اتَّبَعُوهُ وَهَٰذَا النَّبِيءُ وَالَّذِينَ آمَنُوا وَاللَّهُ وَلِيُّ
الْمُؤْمِنِينَ ﴿67﴾ وَدَّت طَّائِفَةٌ مِّنْ أَهْلِ الْكِتَابِ لَوْ يُضِلُّونَكُمْ
وَمَا يُضِلُّونَ إِلَّا أَنفُسَهُمْ وَمَا يَشْعُرُونَ ﴿68﴾ يَا أَهْلَ
الْكِتَابِ لِمَ تَكْفُرُونَ بِآيَاتِ اللَّهِ وَأَنتُمْ تَشْهَدُونَ ﴿69﴾

61. Haƙiƙa wannan (abin ambato,) Lallai shine Labartawa na gaskiya. ba wani abin bautawa da gaskiya sai Allah, haƙiƙa Allah Lallai shine mabuwayi (a cikin mulkinsa,) gwani (a cikin aikinsa).
62. To, in suka bada baya (ga barin imani,) to, haƙiƙa Allah masanine da maɓarnata.

(KALMAR TAUHIDI DA ADDININ ANNABIIBRAHIM)

63. (Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama!) Cene; "Yaku mazowa littafi (Yahudu da Nasare!) kuzo izuwa kalma (wacce take al'amarinta) madaldaici ne tsak-aninmu da ku, Itace; kada mu bautawa kowa sai Allah, kada mu tara komai dashi a cikin bauta, kada sashinmu ya riki sashi iyayen - giji ba Allah ba, " (tamfar daku ,Yahudu da Nasara ku ka riki malamanku,} idan suka bada bayaga barin Tauhidi, to, ku faɗa (musu) "ku shaida mu haƙiƙa musulman haƙiƙa ne".
64. (yayin dayahudu sukace Annabi Ibrahlmu Bayahude ne mu a kan addininsa muke, Nasara ma suka fadi kamar haka, sai Ubangiji yace): "Ya mazowa Httafi! donme ku ke husuma a cikin Annabi Ibrahin (cewa shi a kan addininku yake,) alhali ba a saukar da Attaura da Linjila ba sai bayansa (da zamani mai tsawo, bayan saukarsune kuma Yahudanci da Nasaranci suka samu,) shin ko ba kwa hankaltar (bacin maganarku?)".
65. Ku kula! ku ya waɗannan mutane, kun yi husuma a cikin abindaku ,ke da sani dashi, (Lamar-in Annabi Musa da Annabi Isa Alaihimassalamu, cewa ku a kan addininsu ku ke,) to, donme ku ke jayayya a cikin abinda bakuda sani dashi, (shine sha'anin Annabi Ibrahim Alaihissalamu?) Allah yasan (sha'anin Annabi Ibrahim) ku baku san (shi) ba.
66. (ubangiji ya faɗa saboda kiibiitar da Annabi Ibrahimu, Annabi) Ibrahimu bai kasance Bayahude ko Banasare ba, sai dai shiya kasance a kan addinin totar ne mai kaɗaita Allah, bai kasance daga mushirikai ba".
67. Haƙiƙa mafi cancantar mutane da Annabi Ibrahimu Lallai waɗanda sukabi shi (a zama-ninsa) da wannan Annabi (Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama, saboda dacewarsa dashi cikin mafi yawancin shari'arsa) da waɗanda suka bada gaskiya (na daga al'ummar Annabi Sallallahu alaihi wasalla-ma, sune ya kamata su ce Ibrahimawa ne, baku ba,) Allah shine mataimakin muminai.

(WANI ABU DAGA MATSAYIN AHLIL - KITABI)

68. (Yayin dayahudawa suka kirawo Mu'azu da Huzaifatu da Ammaru, yardar Allah ta tabba-ta garesu izuwa addininsu, sai Allah yace): "Waɗansu mutane daga mazowa littafi sun gurci ɓassheku basa ɓatar da kowa sai kansu (don zunubin ɓatarwar yana kansu, muminai kuwa bazasu saurare su ba,) basa ha-sashen (wannan)".
69. Ya mazowa Littafi! donme ku ke kafirtada ayoyi n Allah (Alƙur'ani wanda yake ɗauke da kamannin Annabi Sallallahu alaihi wasallama) alhali ku kun san (cewa shi gaskiya ne?).

يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ لِمَ تَلۡبِسُونَ ٱلۡحَقَّ بِٱلۡبَٰطِلِ وَتَكۡتُمُونَ ٱلۡحَقَّ وَأَنتُمۡ
تَعۡلَمُونَ ﴿70﴾ وَقَالَت طَّآئِفَةٞ مِّنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ ءَامِنُواْ بِٱلَّذِيٓ
أُنزِلَ عَلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَجۡهَ ٱلنَّهَارِ وَٱكۡفُرُوٓاْ ءَاخِرَهُۥ لَعَلَّهُمۡ
يَرۡجِعُونَ ﴿71﴾ وَلَا تُؤۡمِنُوٓاْ إِلَّا لِمَن تَبِعَ دِينَكُمۡ قُلۡ إِنَّ ٱلۡهُدَىٰ هُدَى ٱللَّهِ
أَن يُؤۡتَىٰٓ أَحَدٞ مِّثۡلَ مَآ أُوتِيتُمۡ أَوۡ يُحَآجُّوكُمۡ عِندَ رَبِّكُمۡۗ
قُلۡ إِنَّ ٱلۡفَضۡلَ بِيَدِ ٱللَّهِ يُؤۡتِيهِ مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ
عَلِيمٞ ﴿72﴾ يَخۡتَصُّ بِرَحۡمَتِهِۦ مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ
ٱلۡعَظِيمِ ﴿73﴾ ۞ وَمِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ مَنۡ إِن تَأۡمَنۡهُ
بِقِنطَارٖ يُؤَدِّهِۦٓ إِلَيۡكَ وَمِنۡهُم مَّنۡ إِن تَأۡمَنۡهُ بِدِينَارٖ لَّا يُؤَدِّهِۦٓ
إِلَيۡكَ إِلَّا مَا دُمۡتَ عَلَيۡهِ قَآئِمٗاۗ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَالُواْ لَيۡسَ عَلَيۡنَا
فِي ٱلۡأُمِّيِّـۧنَ سَبِيلٞ وَيَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ﴿74﴾
بَلَىٰۚ مَنۡ أَوۡفَىٰ بِعَهۡدِهِۦ وَٱتَّقَىٰ فَإِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُتَّقِينَ ﴿75﴾
إِنَّ ٱلَّذِينَ يَشۡتَرُونَ بِعَهۡدِ ٱللَّهِ وَأَيۡمَٰنِهِمۡ ثَمَنٗا قَلِيلًا
أُوْلَٰٓئِكَ لَا خَلَٰقَ لَهُمۡ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ وَلَا يُكَلِّمُهُمُ ٱللَّهُ
وَلَا يَنظُرُ إِلَيۡهِمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَلَا يُزَكِّيهِمۡ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ﴿76﴾

ربع

70. Ya mazowa Littafi! donme ku ke cuɗanya karya da gaskiya (da jirkitawa da kuta ƙarya) kuma ku ke ɓoye gaskiya (ka-mannin Annabi Sallallahu alaihi wasallama) alhali ku kuna sane (da cewa shi gaskiya ne?).

71. Waɗansu mutane daga mazowa Littafi (sune Yahudu)suka faɗa ga sashinsu; "Ku bada gaskiya da abinda aka saukar ga waɗanda suka bada gaskiya, (Alƙur'ani,) farkon rana, ku kafirta dashi ƙarshenta, donsu watakila sa komo (ga barin addininsu).

72. "Kadaku ,gasgatacewa a balwa wani mutum misalin abinda aka baku (na Littafi da Hikiina da Daraja,) sai ko wanda yabi addininku," (Ubangiji yace: Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama, cane dasu;) Haƙiƙar shiriya, shiriyar Allah, ce (wanda shine Musulunci, waninsa kuma ɓata ne,) kada kunia ku gasgatacewa kafirai sa rinjaye ku nan ga Ubangijinku (ranar Alƙiyama don addininku yafi nasu inganci, Ubangiji yace;) "cene" " Haƙiƙa falale a gun Allah take, yana bada ita ga wan-dayaga dama, (ta ina ku ka sami cewa baza a baiwa wani misalin abinda aka baku ba?) Allah mayalwacin falala ne, masanine (da wanda ya cancance ta)".

73. Yana keɓantar wanda yaga dama da rahamarsa, Allah ma/ abucin falala ne maigirma.

(AMANA DA CIK.A ALƘAWARI GUN YAHUDAWA)

74. Akwai daga mazowa Littafi wamda in ka amintar dashi da dukiya mai ɗinbin yawa, zai badashi izuwa gareka (saboda amanarsa, kamar Abdullahi Ibnu Salam. wani Baƙuraishe ya bashi ajiyar wugga [1] ta zinare dubu da maitan, ya bashi ita daidai wadaida,) akwai daga garesu wanda in ka amince shi da dinare ɗaya tal! bazai badashi izuwa gareka ba (saboda ha'incinsa,) sai muddan kana kansa a tsaye, (kamar Ka'abu ɗan Ashrafu, wani Baƙuraishe ya bashi ajiyar zinare saiya danne,) wancananka (rashin bayarwa) saboda su sunce "Uƙuba bata kasance a kanmu ba a cikin Larabawa, (saboda sun halatta zalintar wanda ya saɓa addininsu,) "suna girba ƙarya bisa Ubangiji (a cikin dangana wannan izuwa gareshi) alhali su suna sane (da cewa su maƙaryata ne).

75. Kai! (akwai riƙo a kansu a cikinsu) wanda ya cika da alƙawarinsa (wanda yayi wa Allah ko waninsa,) yaji tsoron Allah, to, haƙiƙa Allah yana son masu tsoransa.

76. (yayin dayahudawa suka musanya kamanninAnnabi a cikin Attaura sai Allah yace): Haƙiƙa waɗanda suka musanyo ɗan tamani ƙanƙani maimakon alƙawarin Allah(izuwa garesu a cikin imani da Annabi Sallallahu alaihi wasalla, da bada amana,) da rantse - rantsensu (a kan ƙarya,) waɗancananka ba rabo a garesu a Lahira, Allah bazaiyi zance dasu ba (don tushi a garesu,) bazaiyi duba (ta jinƙai) izuwa garesu ba, ranar Alƙiyama, bazai tsarkake su ba, azaba mai raɗaɗi ta tabbata a garesu".

1) Wugga : Dan Makodi na Zinare

وَإِنَّ مِنْهُمْ لَفَرِيقاً يَلْوُونَ أَلْسِنَتَهُم بِالْكِتَٰبِ لِتَحْسِبُوهُ
مِنَ الْكِتَٰبِ وَمَا هُوَ مِنَ الْكِتَٰبِ وَيَقُولُونَ هُوَ مِنْ عِندِ اللَّهِ
وَمَا هُوَ مِنْ عِندِ اللَّهِ وَيَقُولُونَ عَلَى اللَّهِ الْكَذِبَ وَهُمْ
يَعْلَمُونَ ﴿77﴾ مَا كَانَ لِبَشَرٍ أَن يُؤْتِيَهُ اللَّهُ الْكِتَٰبَ وَالْحُكْمَ
وَالنُّبُوٓءَةَ ثُمَّ يَقُولَ لِلنَّاسِ كُونُواْ عِبَاداً لِّي مِن دُونِ اللَّهِ
وَلَٰكِن كُونُواْ رَبَّٰنِيِّـۧنَ بِمَا كُنتُمْ تَعْلَمُونَ الْكِتَٰبَ وَبِمَا كُنتُمْ
تَدْرُسُونَ ﴿78﴾ وَلَا يَأْمُرُكُمْ أَن تَتَّخِذُواْ الْمَلَٰٓئِكَةَ
وَالنَّبِيٓـِٔينَ أَرْبَاباً أَيَأْمُرُكُم بِالْكُفْرِ بَعْدَ إِذْ أَنتُم مُّسْلِمُونَ ﴿79﴾
وَإِذْ أَخَذَ اللَّهُ مِيثَٰقَ النَّبِيٓـِٔينَ لَمَا ءَاتَيْنَٰكُم
مِّن كِتَٰبٍ وَحِكْمَةٍ ثُمَّ جَآءَكُمْ رَسُولٌ مُّصَدِّقٌ لِّمَا
مَعَكُمْ لَتُؤْمِنُنَّ بِهِۦ وَلَتَنصُرُنَّهُۥ قَالَ ءَآقْرَرْتُمْ وَأَخَذتُّمْ
عَلَىٰ ذَٰلِكُمْ إِصْرِي قَالُواْ أَقْرَرْنَا قَالَ فَاشْهَدُواْ
وَأَنَا مَعَكُم مِّنَ الشَّٰهِدِينَ ﴿80﴾ فَمَن تَوَلَّىٰ بَعْدَ ذَٰلِكَ
فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ الْفَٰسِقُونَ ﴿81﴾ * أَفَغَيْرَ دِينِ اللَّهِ تَبْغُونَ
وَلَهُۥٓ أَسْلَمَ مَن فِي السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ طَوْعاً وَكَرْهاً وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿82﴾

ثمن

(WANI ABU DAGA ƘARYARSU DA ƘIRƘIRAR'SU BISA ALLAH HAR YAU)

77. Haƙiƙa lallai akwai jama'a daga cikinsu (Ahlalkitabi kamar Ka'abu dan Lashrafu,) suna karkatar da "harshensu da karatun Littafi (ga barin abin a aka saukar izuwa abinda sukajirki" ta shi na daga kamannin Annabi Sallallahu alaihi wasallama,) da waninsa domin ku zaci jirkicaccen nan daga Littafi ne (wanda Allah ya saukar,) alhali kuwa shi baya daga Littafin nan, suna cewa "Shi daga Allah yake," alhali shi badaga Allah yake ba, suna girba ƙarya bisa Ubangi alhali su, sunsan (su maƙaryata ne).

RADDI A BISA AHLIL - KTTABI A CIKIN MUSHIRIKANCINSU DA ALLAH)

78. Bazai yiwu ga BilAdama ba, Allah ya bashi Litafi da fahimtar shari'a da Annabci sannan yace da mutane: "Ku zamo bayina, ba Allah ba. "kai dai zai ce:"Ku zamo masana Allah. masu taƙawa saboda iliminkuda littafi da karantawarku Littafi, (don amfanin sani aiki dashi)".
79. Bazai umarce ku, ku riƙi Mala'ikuda Annanbawa iyayen- giji ba, (kamar yadda Sahawa suka riƙi Mala'iku, Yahudawa Uzairu, Nasara Isa, tsiran Allah da amincinsa su tabbata garesu,) ƙaƙa zai umarce kuda kafirci bayan ku Musulmi ne?

FIFITA MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA A KAN MANZANNI TSIRA DA AMINCAD ALLAH SU TABBATA A GARESU

80. (Ka ambata) z.amanin da Allah ya karɓi alƙawann Annabawa. Lallai abin dana baku na Littafi da hikima, sannan Manzo yazo muku mai gaskatawa da abinda yake tareda ku na daga Lit-tafi da Hikima (shine Annabi Sallallahu alaihi wasallama) Wallahi kwa bada gaskiya dashi, Wallahi kwa taimake shi in kun riske shi (ku da al'ummarku,) Ubangiji yace (dasu) "Kun yi firci da wannan, kun karɓi alƙawarina a kan wancananku? Sukace "Munyi firci", (Ubangiji) "To, ku shaida (wannan bisa kawunankuda mabiyanku,) ni shaida ne taredaku ,(a kan wannan)".
81. To, wanda ya juya baya, bayan wannan alƙawari to, waɗancananka sune fasiƙai.
82. Shin! to, wanin addinin Allah, ku ke nema ne? Alhali duka wanda yake cikin sammai da ƙassaiya jawu gareshi, a ganin dama ko tilas, izuwa gareshi ake komar da ku.

قُلْ ءَامَنَّا بِاللَّهِ وَمَا أُنزِلَ عَلَيْنَا وَمَا أُنزِلَ عَلَىٰ إِبْرَٰهِيمَ
وَإِسْمَٰعِيلَ وَإِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ وَالْأَسْبَاطِ وَمَا أُوتِيَ
مُوسَىٰ وَعِيسَىٰ وَالنَّبِيٓـُٔونَ مِن رَّبِّهِمْ لَا نُفَرِّقُ بَيْنَ أَحَدٍ
مِّنْهُمْ وَنَحْنُ لَهُۥ مُسْلِمُونَ ﴿83﴾ وَمَن يَبْتَغِ غَيْرَ الْإِسْلَامِ
دِينًا فَلَن يُقْبَلَ مِنْهُ وَهُوَ فِي الْآخِرَةِ مِنَ الْخَٰسِرِينَ ﴿84﴾
كَيْفَ يَهْدِي اللَّهُ قَوْمًا كَفَرُوا بَعْدَ إِيمَٰنِهِمْ وَشَهِدُوا أَنَّ الرَّسُولَ
حَقٌّ وَجَآءَهُمُ الْبَيِّنَٰتُ وَاللَّهُ لَا يَهْدِي الْقَوْمَ الظَّٰلِمِينَ ﴿85﴾
أُوْلَٰٓئِكَ جَزَآؤُهُمْ أَنَّ عَلَيْهِمْ لَعْنَةَ اللَّهِ وَالْمَلَٰٓئِكَةِ وَالنَّاسِ
أَجْمَعِينَ ﴿86﴾ خَٰلِدِينَ فِيهَا لَا يُخَفَّفُ عَنْهُمُ الْعَذَابُ وَلَا هُمْ
يُنظَرُونَ ﴿87﴾ إِلَّا الَّذِينَ تَابُوا مِنۢ بَعْدِ ذَٰلِكَ وَأَصْلَحُوا
فَإِنَّ اللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿88﴾ إِنَّ الَّذِينَ كَفَرُوا بَعْدَ إِيمَٰنِهِمْ
ثُمَّ ازْدَادُوا كُفْرًا لَّن تُقْبَلَ تَوْبَتُهُمْ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ
الضَّآلُّونَ ﴿89﴾ إِنَّ الَّذِينَ كَفَرُوا وَمَاتُوا وَهُمْ كُفَّارٌ
فَلَن يُقْبَلَ مِنْ أَحَدِهِم مِّلْءُ الْأَرْضِ ذَهَبًا وَلَوِ افْتَدَىٰ بِهِۦٓ
أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ﴿90﴾

(IMANIN ML'MINAI GA DL'KKAN ANNABAWA, ASBADU KUMA ANNABAWA NE

83. (Ya Annabi Sallallahu alaihi wa-sallama!) Cene (dasu): "Mun bada gaskiya da Allah da abinda aka saukar a garemu da abinda aka saukar ga ibrahimu da Isama'ilu da Ishaku dayaƙubu da "ya"yansa, da abinda aka baiwa Annabi Musa da Isa da Annabawa (tsiran Allah ya tabbata a garesu) daga Ubangijinsu Barna bambancewa tsakanin ɗaya daga garesu, mu masu tsarkakcwar bauta ne gareshi".

(DARAJAR ADDININ MUSULUNCI)

84. (Yayin da wani Musuimi kafircinsa ya bayyana, watau yayi riddaya riskuda kafirai sai Ubangiji yace): "Duka wanda ya nemi wani addini bana Musulunci ba, to, har abada baza a ƙarbadaga gareshi ba, shi a Lahira yana cikin taɓaɓɓu) (don zai koma izuwa wuta abar dauwamawa a gareshi)".

(HUKUNCIN RIDDA, ALLAH YA KIYASHE MU)

85. Allah bazai shiryi mutane da suka kafirta bayan imaninsu ba, da bayan shaidawarsu cewa manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama) gaskiya ne, alhali hujjoji mabayyana (a kan gaskiyarsa) sun zo musu, Allah baya shiriyar mutane kafirai.
86. Waɗancananka sakamakonsu, haƙiƙa tsinewar Allah ta tabbata a garesu, da Mala'iku, da mutane bakiɗaya.
87. madauwama a cikin La'ana (da wuta) baza a sauwaƙe azaba ga barinsu ba, baza a saurara musa (azaba donsu tuba) ba,
88. Sai waɗanda suka tuba bayan wancananka suka kyautata (aikinsu,) to, haƙiƙa Allah mai gafara ne (garesu) mai jinƙai (dasu).

(NAU'O'IN KAFIRAI)

89. (Ubangiji yace a cikin Yahudawa): " haƙiƙa waɗanda suka hafirta (da Annabi Isa bayan gasgatawar su da Annabi Musa) sannan suka ƙara kafircewa (da Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama) har abada Allah bazai karɓi tubansu ba, (a yayin gargara, ai nunfashin ƙarshe,) waɗancananka sune ɓatattu".
90. Haƙiƙa waɗanda suka kafirta suka mutu suna kafirai, to, har abada baza a karbi cikin ƙasa na zinare badaga ɗayansu, kodazaiyi fansa dashi, waɗancananka, azaba mai raɗaɗi ta tabbata a garesu, basu da masu hana musu azabar Allah.

(CIYARWA)

حزب

۞ لَن تَنَالُواْ اُ۬لْبِرَّ حَتَّيٰ تُنفِقُواْ مِمَّا تُحِبُّونَۖ وَمَا تُنفِقُواْ مِن شَےْءٖ
فَإِنَّ اَ۬للَّهَ بِهِۦ عَلِيمٞۖ ﴿91﴾ كُلُّ اُ۬لطَّعَامِ كَانَ حِلّاٗ لِّبَنِيٓ إِسْرَآءِيلَ
إِلَّا مَا حَرَّمَ إِسْرَآءِيلُ عَلَيٰ نَفْسِهِۦ مِن قَبْلِ أَن تُنَزَّلَ اَ۬لتَّوْرَيٰةُۖ قُلْ فَأْتُواْ
بِالتَّوْرَيٰةِ فَاتْلُوهَا إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَۖ ﴿92﴾ فَمَنِ اِ۪فْتَرَيٰ عَلَى اَ۬للَّهِ
اِ۬لْكَذِبَ مِنۢ بَعْدِ ذَٰلِكَ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ اُ۬لظَّٰلِمُونَۖ ﴿93﴾ قُلْ صَدَقَ اَ۬للَّهُۖ
فَاتَّبِعُواْ مِلَّةَ إِبْرَٰهِيمَ حَنِيفاٗۖ وَمَا كَانَ مِنَ اَ۬لْمُشْرِكِينَۖ ﴿94﴾ إِنَّ أَوَّلَ
بَيْتٖ وُضِعَ لِلنَّاسِ لَلَذِے بِبَكَّةَ مُبَٰرَكاٗ وَهُديٗ لِّلْعَٰلَمِينَ ﴿95﴾
فِيهِ ءَايَٰتُۢ بَيِّنَٰتٞ مَّقَامُ إِبْرَٰهِيمَۖ ﴿96﴾ وَمَن دَخَلَهُۥ كَانَ ءَامِناٗۖ
وَلِلَّهِ عَلَى اَ۬لنَّاسِ حَجُّ اُ۬لْبَيْتِ مَنِ اِ۪سْتَطَاعَ إِلَيْهِ سَبِيلاٗۖ وَمَن كَفَرَ
فَإِنَّ اَ۬للَّهَ غَنِيٌّ عَنِ اِ۬لْعَٰلَمِينَۖ ﴿97﴾ قُلْ يَٰٓأَهْلَ اَ۬لْكِتَٰبِ لِمَ تَكْفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ
اِ۬للَّهِ وَاللَّهُ شَهِيدٌ عَلَيٰ مَا تَعْمَلُونَۖ ﴿98﴾ قُلْ يَٰٓأَهْلَ اَ۬لْكِتَٰبِ
لِمَ تَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ اِ۬للَّهِ مَنْ ءَامَنَ تَبْغُونَهَا عِوَجاٗ
وَأَنتُمْ شُهَدَآءُ وَمَا اَ۬للَّهُ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعْمَلُونَۖ ﴿99﴾
يَٰٓأَيُّهَا اَ۬لَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن تُطِيعُواْ فَرِيقاٗ مِّنَ اَ۬لَّذِينَ
أُوتُواْ اُ۬لْكِتَٰبَ يَرُدُّوكُم بَعْدَ إِيمَٰنِكُمْ كَٰفِرِينَۖ ﴿100﴾

91. Bazaku sami sakamakon ɗa'a ba, (shine Aljanna) sai kun ciyar daga abindaku ,ke so (na da ga dukiyoyinku).

92. Abindaku ,ka ciyar na kowane abu, to, haƙiƙa Allah masanine dashi.

(ƘARYAR YAHUDAWA A CIKIN HARAMTA BA'ALIN ABINCI)

93. (Yayin dayahudu sukace dashi, kana riyawa cewa kai a kan addinin Annabi Ibrahimu ka k e. shi ko baya cin naman raƙumi da nonon sa, sai Ubangiji yace): "Dukkan abinci ya kasanc e halal gu Bani'isra'ila, sai abinda yaƙubu ya haramta a kan kansa, (shine raƙumi, yayin da ciwon Irƙunnasa ya same shi, yayi al-washin in an warkar dashi bazai sake cin naman raƙu mi ba, tareda kasancewarsa mafi soyiwar nama a gareshi dashi da "ya"yansa da zuriyarsa) t un gaban ba a saukar da Attaura ba, (to, wancananka bayan Annabi Ihrahimu ne, saboda ha ka bai kasance haram ba a zamaninsa.) cene (dasu) "Ku zoda Attaura ku karanta ta (saboda gaskiyar maganar ku ta bayyana) in kun kasance magasgata (a cikinsa", sai sukayi ƙus, bas u zoda ita ba).

94. (Uhangiji yace): "Duka wanda ya ƙirƙiri ƙarya bisa Ubangiji bayan wancananka (bayyana r hujja dacewa haramcin nan ya kasance ne ta jihar Yaƙubu bazamanin Annabi Ihrahim ba.) to waɗancananka sune masu kelare gaskiya (izuwa ƙarya)".

95. Cene) "Allah yagasgata (cikin dukkan abinda ya bada Labari dashi.) saikubi addinin Anna bi Ibrahimu (wanda nake kansa) totar, bai kasance daga mushirikai ba".

(ALƘIBLA TA FARKO A DUNIYA DA GIRMAN DAKIN ALLAH MAI ALFARMA KUMA DA WAJABCIN HAJJI

96. (Yayin da sukace "alƙibarmu ta gabaci alƙiblarku sai Allah yace): " haƙiƙa farkon daƙi da aka ajiye shi (mabauta) ga mutane (a cikin kasa,) Lallai wanda yake a Bakka (an ambace ta Bakka saboda tana dandaƙe wuyayikan jabberai, Mala'iku sun gina shi gaban halittar Anna bi Adamu da shekara dubu biyu, an ajiye Masjidul -Aƙsa bayansa da shekara arba'in, a ciki n hadisi: haƙiƙa shine farkon abinda ya bayyana a fuskar ruwa yayin halittar sammai da kas sai yana kunta fara, aka shimfiɗe ƙasa daga ƙarƙashinsa) yana mai albarka, shiriyaga talikai (domin shine alƙiblarsu)".

97. Akwai ayoyi mabayyana a cikinsa (yana daga cikinta Maƙamu Ibrahima dutsen daya tsaya kansa yayin gina ɗaki, di- gadigansa suka nitse a cikinsa, yana sama dashiyana ƙasa dashi watau shine tsaninsa. da zamansa har yau yana nan tareda tsawon zama da shafe - shafenha nnayen masu nenan albarka tasa a kansa, yana daga ayoyin nan ninninkawar hasana [1] a ci kinsa, tsuntsu bayabi ta samansa, sai ko idan bashi da lafiyaya wuce don neman waraka) wa nda ya shige shiya kasance amintacee daga kisa ko zalunci ko wanin wannan. Nufantar ɗak in Allah yana ga Allah a kan mutane, wanda ya sami dama izuwa gareshi, (guzuri ishasshe da abin hawa amintacce dashirye - shiryen da suka zama dole kamar fasfo da waninsa). Wa nda ya kafirtada Allah ko abinda ya wajabta na hajji da waninsa, to, haƙiƙa allah mawadaci ne ga barin talikai, (mutum da aljan da Mala'ikuda waninsu, mawadaci ne ga barin su da iba darsu).

(AHLIL - KITABI DA TAURIN KANSU DA MUMMUNAN TANADINSU GA MUSUL UNCI)

98. Cene: "Ya Ahlal - kitabi' donme ku ke kafircewa da ayoyin Allah (Alƙur'ani)? Allah shaid a ne a kan abindaku ,ke aikatawa (zaiyi muku sakamako a kansa)".

99. Cene: "Ya Ahlal - kitabi! donme kuke juyar da wanda ya bada gaskiyaga barin addinin Al lah, kuna nemanta a fanɗare alhali ku kuna masana (da cewa addini yardajje dai shine Dinil -Islam, tamtar dayakc cikin Littafinku?) Allah ba marafkani bane ga barin abindak, ke aika tawa (na kafirci da ƙaryatawa, yanayi muku jinkiri ne kawal zuwa Lokacin ku don sakama ko)".

(FUSKANTARWA DA GARGADI)

100. (Yayin da ba'alin Yahudawa ya wuce a bisa Ausu da Hazraju. gamá kansu yafisatar dashi, saiya tuno musu basasassu ta jahiliyya, sai suka tayar da hankalinsu, sai Allah yace): "Ya waɗanda suka bada gaskiya idan kun biyewa Jama'a daga waɗanda aka basu Littafi, sa mayar daku ,kafirai bayan imaninku.

1) Sakamakon alheri

وَكَيۡفَ تَكۡفُرُونَ وَأَنتُمۡ تُتۡلَىٰ عَلَيۡكُمۡ ءَايَٰتُ ٱللَّهِ
وَفِيكُمۡ رَسُولُهُۥۗ وَمَن يَعۡتَصِم بِٱللَّهِ فَقَدۡ هُدِيَ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ﴿101﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ حَقَّ تُقَاتِهِۦ وَلَا تَمُوتُنَّ إِلَّا وَأَنتُم
مُّسۡلِمُونَ ﴿102﴾ وَٱعۡتَصِمُواْ بِحَبۡلِ ٱللَّهِ جَمِيعٗا وَلَا تَفَرَّقُواْۚ وَٱذۡكُرُواْ
نِعۡمَتَ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ إِذۡ كُنتُمۡ أَعۡدَآءٗ فَأَلَّفَ بَيۡنَ قُلُوبِكُمۡ
فَأَصۡبَحۡتُم بِنِعۡمَتِهِۦٓ إِخۡوَٰنٗا وَكُنتُمۡ عَلَىٰ شَفَا حُفۡرَةٖ مِّنَ ٱلنَّارِ
فَأَنقَذَكُم مِّنۡهَاۗ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمۡ ءَايَٰتِهِۦ لَعَلَّكُمۡ تَهۡتَدُونَ ﴿103﴾
* وَلۡتَكُن مِّنكُمۡ أُمَّةٞ يَدۡعُونَ إِلَى ٱلۡخَيۡرِ وَيَأۡمُرُونَ بِٱلۡمَعۡرُوفِ ثمن
وَيَنۡهَوۡنَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ﴿104﴾ وَلَا تَكُونُواْ
كَٱلَّذِينَ تَفَرَّقُواْ وَٱخۡتَلَفُواْ مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلۡبَيِّنَٰتُۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ
لَهُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ ﴿105﴾ يَوۡمَ تَبۡيَضُّ وُجُوهٞ وَتَسۡوَدُّ وُجُوهٞۚ فَأَمَّا
ٱلَّذِينَ ٱسۡوَدَّتۡ وُجُوهُهُمۡ أَكَفَرۡتُم بَعۡدَ إِيمَٰنِكُمۡ فَذُوقُواْ ٱلۡعَذَابَ
بِمَا كُنتُمۡ تَكۡفُرُونَ ﴿106﴾ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ ٱبۡيَضَّتۡ وُجُوهُهُمۡ
فَفِي رَحۡمَةِ ٱللَّهِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿107﴾ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱللَّهِ
نَتۡلُوهَا عَلَيۡكَ بِٱلۡحَقِّۗ وَمَا ٱللَّهُ يُرِيدُ ظُلۡمٗا لِّلۡعَٰلَمِينَ ﴿108﴾

101. "YaYaku ke kafirta alhali ku ana karanta ayoyin Alluh a gareku, nianzonsa yana cikinku? Duka wanda ya ƙanƙame Atlah haƙiƙa an shirye shi izuwa tafarki madaidaici".

102. Ya waɗanda suka bada gaskiya! kuji tsoron Allah haƙiƙa r tsoronsa, (shinc a bi shi kada a saɓe shi, a gode masa kada a katirce masa. a ambace shi kada a mance shi, sai suka ce; "Ya Rasulallahi wa zai iya haka a cikinmu?" Sai akayi masu cikakken bayani da faɗin Ubangiji):"Kuji tsoron Allah gwargwadon ikonku. kadaku ,mutu tacc kuna Musulmin gaskiya".

103. Ku kankame igiyar Allah, (ad-dininsa) bakiɗaya. kada kuyi daban - daban (,bayan Musulunci,) ku ambaci ni'imar Ubangiji a gareku. (Yaku Ausu da Hazaraju da sauran Musulmi.) zamanin daku ,ka kasance magauta juna (gaban Musulunci) sai ku ka zama "yan'uwa (a cikin addini da taimako) saboda ni'imar Allah, kLin kasance a gaɓar rami na wuta (ba abinda ya hana shigar ku ciki sai in baku mutu kafirai ba,) ya tsamo ku daga gareta (da imani) tamfar da Allah yayi muku bayanin abinda aka ambata gareku yake muku bayanin ayoyinsa, don haƙiƙa ku shiriya.

(UMARNI DA ABIN SANI A SHARI'A DA HANI GA AIKIN MUNKARI[1]

104. Al'umma ta samu daga cikinkuda zasu rlnga kira izuwa Musulunci, suyi umarni da abin sani (a shari'a) suyi hani ga barin munkari, waɗancananka (masu kira izuwa Musulunci da Amm da Nahyu sunc marabauta, (wannan umarni yana kama macancancinsa ba kowane mutun ba).

(WAH DA TUL ISLAMIYYA WATO (TSORATARWA DAGA RARRABA)

105. Kadaku ,zamo tamfar waɗanda sukayi daban - daban (ga barin addininsu,} suka sassaba (a cikinsa,) bayan hujjoji maɓayyana sun zo musu (sune Yahudu da Nasara,) waɗancananka azaba mai girma tana garesu.

106. Ranar da wasu fuskoki suke fa-ranta, wasu tuskoki suke duhunta, (Ranar Alƙiyama) amman waɗanda fuskokinsu suka duhunta (sune kaflrai, za ajefa su a wuta, a urusta su da faɗin):"Kun kafirta ne bayan Imaninku ranar ruƙon alƙawari? to, ku ɗanɗani azaba saboda kafircin dakuka aikata".

107. Amma waɗanda fuskokinsu ta faranta, (sune muminai) to, suna cikin rahamar Allah (Aljanna) su madauwama nc a cikinta.

108.Waɗannan (ayoyi) ayoyin Allah ne, muka karanta su a gareka (Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama) da gaskiya, Allah baya nufin zalunci ga talikai (ya riƙe su bada Laifi ba).

وَلِلَّهِ مَا فِي السَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ وَإِلَى اللَّهِ تُرْجَعُ
الْأُمُورُ (109) كُنتُمْ خَيْرَ أُمَّةٍ أُخْرِجَتْ لِلنَّاسِ تَأْمُرُونَ
بِالْمَعْرُوفِ وَتَنْهَوْنَ عَنِ الْمُنكَرِ وَتُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ
وَلَوْ ءَامَنَ أَهْلُ الْكِتَٰبِ لَكَانَ خَيْرًا لَّهُم مِّنْهُمُ الْمُؤْمِنُونَ
وَأَكْثَرُهُمُ الْفَٰسِقُونَ (110) لَن يَضُرُّوكُمْ إِلَّا أَذًى وَإِن يُقَٰتِلُوكُمْ
يُوَلُّوكُمُ الْأَدْبَارَ ثُمَّ لَا يُنصَرُونَ (111) ضُرِبَتْ عَلَيْهِمُ
الذِّلَّةُ أَيْنَ مَا ثُقِفُوا إِلَّا بِحَبْلٍ مِّنَ اللَّهِ وَحَبْلٍ مِّنَ النَّاسِ
وَبَاءُو بِغَضَبٍ مِّنَ اللَّهِ وَضُرِبَتْ عَلَيْهِمُ الْمَسْكَنَةُ ذَٰلِكَ
بِأَنَّهُمْ كَانُوا يَكْفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ اللَّهِ وَيَقْتُلُونَ الْأَنْبِئَاءَ
بِغَيْرِ حَقٍّ ذَٰلِكَ بِمَا عَصَوا وَّكَانُوا يَعْتَدُونَ (112)
* لَيْسُوا سَوَاءً مِّنْ أَهْلِ الْكِتَٰبِ أُمَّةٌ قَائِمَةٌ يَتْلُونَ
ءَايَٰتِ اللَّهِ ءَانَاءَ الَّيْلِ وَهُمْ يَسْجُدُونَ (113) يُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ وَالْيَوْمِ
الْأٓخِرِ وَيَأْمُرُونَ بِالْمَعْرُوفِ وَيَنْهَوْنَ عَنِ الْمُنكَرِ
وَيُسَٰرِعُونَ فِي الْخَيْرَٰتِ وَأُوْلَٰٓئِكَ مِنَ الصَّٰلِحِينَ (114) وَمَا تَفْعَلُوا
مِنْ خَيْرٍ فَلَن تُكْفَرُوهُ وَاللَّهُ عَلِيمٌ بِالْمُتَّقِينَ (115)

ربع

109. Abinda yake sammai da ƙassaina Allah ne (mallaka da halittada bauta,) izuwa Allah al'aniura suke komawa.

(FIFIKON AL'UMMAR ANNABI VIUHAMMADU SALLALLAHU ALAI-IIWASALLAMA A KAM WATANTA, YAHUDU DA WADANSUNSU)

110. (Ya Ummata Muhainmadin Sallallahu alaihi wasallama!) kun kasance (a cikin sanin Allah) mafifitan al'umma da aka bayyanata, kuna umarni da abin sani (a shari'a) kuna hani da abin ƙi (a shari'a), kun bada gaskiya da Allah, (wannan aya ta turmuza hancin ƙaumiyya watau ƙabilanci,) da Ahlil - kitabi sun bada gaskiya daya kasance mafi amfani garesu, akwai muminai daga cikinsu, (Kamar Abdullahi bini Salam yardar Allah ta tabbata gareshi, da sahabbansa).yawaicinsu kafirai ne.

111. (yahudawa) bazasu cuce ku har abada da komai ba, (Yaku jamar'ar Musulmi!) sai cutada harshe, zagi da narko,) in sun yaƙe ku sa juya muku baya (aguje,) sannan kuma baza a taimake su (a kan ku ba watau ku za a taimaka a kansu).

112. An buga ƙasƙanta a kansu inda duk aka same su, (ba girma garesu ba hanuwa) sai ko tareda igiya daga Allah, (imani) da igiya daga mutane (ƙudure amana, akwai albishir ga Musulmi cikin wannan aya ta samun nasara a kan Yahudawa bisa yaƙi n da ake tsakaninsu da Larabawa a yau) sun komo da fushi na daga Allah, an buga talauci a kansu, wancananka saboda sun sun kasance suna kafircewa da ayoyin Allah suna kafircewa da ayoyin Allah suna kashe Annabawa ba gaira badalili, wancananka saboda sun sabi umarnin Allah kuma sun kasance suna shishshigi (ƙetare halal izuwa haram).

(MUMINAI DAGA AHLIL- KITABI)

113. (Ahlil - kitabi) badaidai suke ba, akwai daga Ahlil - kitabi al'umma madaidaiciya (a kan gaskiya, kamar Addullahi bini Salam yadar Allah ta tabbata a gareshi da abokansa) suna ka-ranta ayoyin Allah a cikin sa'o'in dare, alhali su suna masu sallah.

114. Suna bada gaskiya da Allah da ranar Lahira. suna umarni da abin sani (a shari'a) suna hani ga aikin munkari, suna gaggawa a cikin alhairai, waɗancananka, (ababan kamantawa da abinda aka ambata) suna daga salihai, (akwai daga cikinsu waɗanda ba haka suke ba, basa cikin salihai).

115. Duk abindaku ,ka aikata na alhairi, baza a ƙi saka muku ba, Allah masanine da masu tsoransa.

(KAFIRAI DA AYYUKANSU RANAR ALƘIYAMA)

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لَن تُغۡنِىَ عَنۡهُمۡ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُهُم مِّنَ
ٱللَّهِ شَيۡـًٔا ۖ وَأُو۟لَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِ ۚ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿116﴾
مَثَلُ مَا يُنفِقُونَ فِى هَٰذِهِ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا كَمَثَلِ رِيحٍ فِيهَا صِرٌّ
أَصَابَتۡ حَرۡثَ قَوۡمٍ ظَلَمُوٓا۟ أَنفُسَهُمۡ فَأَهۡلَكَتۡهُ ۚ وَمَا ظَلَمَهُمُ ٱللَّهُ
وَلَٰكِنۡ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ﴿117﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تَتَّخِذُوا۟
بِطَانَةً مِّن دُونِكُمۡ لَا يَأۡلُونَكُمۡ خَبَالًا وَدُّوا۟ مَا عَنِتُّمۡ
قَدۡ بَدَتِ ٱلۡبَغۡضَآءُ مِنۡ أَفۡوَٰهِهِمۡ وَمَا تُخۡفِى صُدُورُهُمۡ أَكۡبَرُ ۚ
قَدۡ بَيَّنَّا لَكُمُ ٱلۡءَايَٰتِ ۖ إِن كُنتُمۡ تَعۡقِلُونَ ﴿118﴾ هَٰٓأَنتُمۡ أُو۟لَآءِ
تُحِبُّونَهُمۡ وَلَا يُحِبُّونَكُمۡ وَتُؤۡمِنُونَ بِٱلۡكِتَٰبِ كُلِّهِۦ
وَإِذَا لَقُوكُمۡ قَالُوٓا۟ ءَامَنَّا وَإِذَا خَلَوۡا۟ عَضُّوا۟ عَلَيۡكُمُ ٱلۡأَنَامِلَ
مِنَ ٱلۡغَيۡظِ ۚ قُلۡ مُوتُوا۟ بِغَيۡظِكُمۡ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ﴿119﴾
إِن تَمۡسَسۡكُمۡ حَسَنَةٌ تَسُؤۡهُمۡ وَإِن تُصِبۡكُمۡ سَيِّئَةٌ يَفۡرَحُوا۟ بِهَا ۖ
وَإِن تَصۡبِرُوا۟ وَتَتَّقُوا۟ لَا يَضُرُّكُمۡ كَيۡدُهُمۡ شَيۡـًٔا ۗ
إِنَّ ٱللَّهَ بِمَا يَعۡمَلُونَ مُحِيطٌ ﴿120﴾ ۞ وَإِذۡ غَدَوۡتَ مِنۡ أَهۡلِكَ ثمن
تُبَوِّئُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ مَقَٰعِدَ لِلۡقِتَالِ ۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿121﴾

116. Haƙiƙa waɗanda suka kafirta, dukiyoyinsu da "ya"yansu bazasu ije musu komai ba (na daga azabar) Allah, kuma waɗancananka sune "yan wuta, su masu dauwama ne a cikinta.

117. Misalin abinda kafirai suke ciyarwa a cikin wannan rayuwa ta duninya, (suke ciyarwa a cikin gabada Annabi Sallallahu alaihi wasallama, ko sadaka, da (makamancinta) Kamar misalin iskace da zafi mai tsanani yake cikinta ta samu hatsin mutane da suka zalunci kansu (da kafirci da saɓo,) saita halakar dashi, (hakana waɗannan mutane abinda suka ciyar bazai amfane su ba, Allah bai zalunce su ba, (da tozartar abinda suka ciyar,) saida kansu kaɗai suke zalunta, (da kafirci wanda ya wajabta tozartar aiki).

(ABOTAKAR MUMINAI GA KAFIRAI DA HADARIN TA)

118. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! kadaku ,riƙi waninku (Yahudu, Nasara da munafikai) (ba sake[1] ciki), bazasu taƙaita muku a cikin ɓarna ba, suna gu-rin wahaltuwar ku. haƙiƙa gaba (da ku) ta bayyana daga bakunansu, (da cin mutuncinku, da tsinkayar da munafikai a cikin sirrin ku,) abinda ƙirajansu ta ɓoye (na gaba) yafi girma, haƙiƙa mun bayyana muku ayoyi (a bisa adawarsu,) in kun kasance kun hankalci (wannan, to, kadaku ,daukake su).

119. Ku! ku lura Yaku waɗannan (Muminai) kuna son su, (saboda zumuncin tsakaninku, da abokantaka) su ko basa son ku, (saboda saɓawar addinku ku,) kuna ba du gaskiya da littafi dukkansa, in sun gamu daku ,sukan ce:"Mun bada gaskiya", in sun kaɗaita sukan ciji "yanyatsu a kanku saboda (tsananin) fushi, (saboda abinda suke gani na daga haɗa kanku,) cene (dasu) "Ku mutu da fushinku, (bazaku ga abindazai faranta muku ba har abada) haƙiƙa Ubangiji inasanine da abinda yake cikin zukata".

120. Idan ni'ima ta same ku (Kamar Nasara da ganima) saita baƙanta musu, idan musifa ta same ku, (kamar risɓawa karyewar yaƙi da fari) sai suyi murna da ita, (sun isa mutuka a cikin gabada ku, donme zaku daukake su? kuyi ne sa dasu, idan kukai haƙuri bisa cutar dasuke muku, kukaji tsoran Allah (a cikin daukakar su da waninta,) kaidinsu bazai cuce ku komai ba, haƙiƙa Allah makewayin sanine da abinda suke aikatawa.

(ABINDA ALLAH YA SAUKAR NA DAGA RISBAWAR YAƘI DA NASARAR YAƘIN UHUDU? DA BADAR)

121. (Ya Annabi Sallallahu alaihi wa wasallama' ka ambata) zamanin da kayi sammako daga Madina kana tsayar da muminai matsayai na yaƙi, Ubangiji mai ji ne (da maganganunkuda haluluwanku,) masanine (dasu).

1) Bur'ga min asirinka

إِذْ هَمَّت طَّآئِفَتَانِ مِنكُمْ أَن تَفْشَلَا وَاللَّهُ وَلِيُّهُمَا
وَعَلَى اللَّهِ فَلْيَتَوَكَّلِ الْمُؤْمِنُونَ ﴿122﴾ وَلَقَدْ نَصَرَكُمُ اللَّهُ بِبَدْرٍ
وَأَنتُمْ أَذِلَّةٌ فَاتَّقُوا اللَّهَ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿123﴾ إِذْ تَقُولُ
لِلْمُؤْمِنِينَ أَلَن يَكْفِيَكُمْ أَن يُمِدَّكُمْ رَبُّكُم بِثَلَاثَةِ ءَالَافٍ
مِّنَ الْمَلَائِكَةِ مُنزَلِينَ ﴿124﴾ بَلَىٰ إِن تَصْبِرُوا وَتَتَّقُوا وَيَأْتُوكُم
مِّن فَوْرِهِمْ هَٰذَا يُمْدِدْكُمْ رَبُّكُم بِخَمْسَةِ ءَالَافٍ مِّنَ الْمَلَائِكَةِ
مُسَوَّمِينَ ﴿125﴾ وَمَا جَعَلَهُ اللَّهُ إِلَّا بُشْرَىٰ لَكُمْ وَلِتَطْمَئِنَّ قُلُوبُكُم بِهِ
وَمَا النَّصْرُ إِلَّا مِنْ عِندِ اللَّهِ الْعَزِيزِ الْحَكِيمِ ﴿126﴾ لِيَقْطَعَ طَرَفًا
مِّنَ الَّذِينَ كَفَرُوا أَوْ يَكْبِتَهُمْ فَيَنقَلِبُوا خَائِبِينَ ﴿127﴾ لَيْسَ
لَكَ مِنَ الْأَمْرِ شَيْءٌ أَوْ يَتُوبَ عَلَيْهِمْ أَوْ يُعَذِّبَهُمْ فَإِنَّهُمْ
ظَالِمُونَ ﴿128﴾ وَلِلَّهِ مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ يَغْفِرُ لِمَن يَشَاءُ وَيُعَذِّبُ
مَن يَشَاءُ وَاللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿129﴾ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُوا
لَا تَأْكُلُوا الرِّبَا أَضْعَافًا مُّضَاعَفَةً وَاتَّقُوا اللَّهَ لَعَلَّكُمْ
تُفْلِحُونَ ﴿130﴾ وَاتَّقُوا النَّارَ الَّتِي أُعِدَّتْ لِلْكَافِرِينَ ﴿131﴾
وَأَطِيعُوا اللَّهَ وَالرَّسُولَ لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ ﴿132﴾

122. Yayin da jama'a biyu daga cikinku, (Bunu -Salmatada Bunu - Harisata, fikafikan yaƙi.) suka nufi su karaya (Allah ya taimake su,) Allah ne mataimakinsu, duka muminai su dogara ga Allah kaɗai.
123. (Yayin da aka risɓa su don tinasar dasu da ni'imarsa, sai Allah yace): " Haƙiƙa Allah ya taimake ku a badar (guri ne tsakanin Makka da Madina) alhali kuna raunana (da karancin runduna da makami,) to, kuji tsoron Allah don ku godewa (ni'imominsa/'.
124. Zamanin da kake faɗa ga muminai (don kwantar da hankalinsu): "Shin bazai ishe ku ba Ubangijinku ya taimake kuda dubu uku na Mala'iku abahan saukarwa?"
125. "Na'am ya ishe mu," (Ubangiji yace): "In ku ka daure (bisa gamo da magauta) ku kaji tsoron Allah (a cikin saɓawa) mushirikai sukazo muku a cikin Lokocinsu. wannan. Ubarigijinku ya kare kuda dubu biyar na Mata'iku niayu rawuna Launi -Launi".
126. Allah bai sanya wannan ninduna ba sai don albishir gareku (da taimako) kuina don zukatan ku ta nutsu dashi (kada kuyi raki daga yau don yawan magautada kisan ku,) taiinaku bai kasance ba illa daga Allah, mabuwayi mai hikirna, (bada yawan runduna ba).
127. (Ya taimake ku ne) donya halakar dayanki daga waɗanda suka kafirta (da kisa da ribacewa) ko ya wulakantar dasu (da risɓawa,) su komo taɓaɓɓu.

(ROTSE FUSKAR ANNABI SALLALLAHLI ALAIHI WASALLAMA DA KARYA HAƘORINSA)

128. (Yayin da kafirai suka karya haƙoran gabana Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama suka rotsa fuskarsa ranar Uhu-du, yace: "ƙaƙa mutanen da suka kwaba fuskar Annabinsu dajini zasu tsira?" Sai Allah yace): "Baka da komai cikin wan-nan Lamari, (Lamari na Allah ne sai ka haƙura) har izuwa Allah ya karɓi tubansu (da musulunci) ko yayi musu azaba, to, haƙiƙa su azzalumai ne (da Kafirci)".
129. Abinda yake sammai da ƙassaina Allah ne (mallaka da halittada baula,) yana gafara ga wanda yaga damar (yi masa gafara) yana azaba ga wanda yaga damar (yi masa azaba,) Allah mai gafara ne (ga waliyansa) mai jinkaine (ga ma'aboia ɗa'arsa).

(HANI GA CTN RIBADASHIRYAR DA MUMINAI DA SAKAMAKONSLH

130. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! kadaku ,ci ribaninke- ninke abin ninnlnkawa (kuyi ƙari a cikin dukiya yayin saukar ajali kujiinkirta nema,) kii tsoraci Allah don haƙiƙa ku rabauta.
131. Kuji tsoron wuta wacce aka tanada ga kafirai.
132. Kubi Allah da manzonsa don haƙiƙa a jiƙan ku.

ربع

۞ وَسَارِعُوٓاْ إِلَىٰ مَغۡفِرَةٖ مِّن رَّبِّكُمۡ وَجَنَّةٍ عَرۡضُهَا ٱلسَّمَٰوَٰتُ
وَٱلۡأَرۡضُ أُعِدَّتۡ لِلۡمُتَّقِينَ ١٣٣ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ فِي ٱلسَّرَّآءِ وَٱلضَّرَّآءِ
وَٱلۡكَٰظِمِينَ ٱلۡغَيۡظَ وَٱلۡعَافِينَ عَنِ ٱلنَّاسِۗ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٣٤
وَٱلَّذِينَ إِذَا فَعَلُواْ فَٰحِشَةً أَوۡ ظَلَمُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ ذَكَرُواْ ٱللَّهَ
فَٱسۡتَغۡفَرُواْ لِذُنُوبِهِمۡ وَمَن يَغۡفِرُ ٱلذُّنُوبَ إِلَّا ٱللَّهُ
وَلَمۡ يُصِرُّواْ عَلَىٰ مَا فَعَلُواْ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ١٣٥ أُوْلَٰٓئِكَ
جَزَآؤُهُم مَّغۡفِرَةٞ مِّن رَّبِّهِمۡ وَجَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا
ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ وَنِعۡمَ أَجۡرُ ٱلۡعَٰمِلِينَ ١٣٦ قَدۡ
خَلَتۡ مِن قَبۡلِكُمۡ سُنَنٞ فَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَٱنظُرُواْ
كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُكَذِّبِينَ ١٣٧ هَٰذَا بَيَانٞ لِّلنَّاسِ
وَهُدٗى وَمَوۡعِظَةٞ لِّلۡمُتَّقِينَ ١٣٨ وَلَا تَهِنُواْ وَلَا تَحۡزَنُواْ
وَأَنتُمُ ٱلۡأَعۡلَوۡنَ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ١٣٩ إِن يَمۡسَسۡكُمۡ
قَرۡحٞ فَقَدۡ مَسَّ ٱلۡقَوۡمَ قَرۡحٞ مِّثۡلُهُۥۚ وَتِلۡكَ ٱلۡأَيَّامُ
نُدَاوِلُهَا بَيۡنَ ٱلنَّاسِ وَلِيَعۡلَمَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
وَيَتَّخِذَ مِنكُمۡ شُهَدَآءَۗ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٤٠

133. Kuyi gaggawa izuwa gafara daga Ubangijinkuda aljanna, da fađin ta sammai da ƙassai (ai kamar fađin su daza a sada đayarsu da đayar,) an tanaje ta ga masu tsoron Allah.

134. (Su ne) wađanda suke ciyarwa a cikin (đa'ar Allah) a cikin sauki da tsanani da masu hađiye tushi (tareda iko a kan zartar dashi,) masu rangwame ga barin wađanda suka zalunce su. (basayi musu uƙuba,) Allah yana -son masu kyakkyawan aiki, da (irin wađannan ayyuka).

135. Da wađanda idan sun aikata mummunan aiki (kabira kamar zina,) ko suka zalunci kawukansu, (da abinda yake koma -bayansu, sagira kamar sunba,) saisu ambaci Allah da (azabar-sa,) saisu nemi gafara ga zunu-bansu, ba mai gafarta zunubai sai Allah, basa zarcewa a kan abinda suka aikata alhali su suna sane (da cewa abin nan da suka aikata sabo ne).

136. Wađancananka sakamakonsu gafara daga Ubangijinsu, da Aljannatai da ƙoramu suke kwarara ƙarƙashinta madauwama a cikinta, madalla Ladan ma'aikata (wannan Lada!).

(AL'ADAR ALLAH A CIKIN HALITTADA AƘIBAR [1] MASU TSORON ALLAH)

137. (Yayiri da aka sami risbawa a yaƙin Uhudu sai Allah yace):" Haƙiƙa al'adun Ubangiji a cikin kafirai sun wuce gaban ku, (shine yayi masu sauraro kuma ya riƙe su,) to, kuyi tafiya (ku muminai) a cikin ƙasa ku duba ƙaƙa ƙarshen masu ƙaryata (manzanni) ya kasance?" (An halakar dasu, to, kada kuyi baƙin ciki ga rinjayar da sukayi muku, an jinkirta musune kawai kafin a riƙe su).

138. Wannan (Alƙur'ani) bayanine ga mutane (dukkansu,) shiriya ne daga bata, gargađi ne ga masu jin tsoron Allah (duga cikin su).

139. Kada kuyi rauni (ga barin yaƙin kafirai,) kada kuyi baƙin ciki (bisa abinda ya same ku Uhudu ko waninsa) kune mafiya đaukaka (da rinjaye a kansu) in kun kasance muminai (da Allah imanin gaskiya).

140. Idan miki ya same ku (a Uhudu,) to, haƙiƙa miki irinsa ya sami kaflran (a Badar,) wancananka kwanika muna juya ta ga mutane, (yau ga wađannan gobe ga wađancan, donsu wa'azantu, kuma) don Allah ya nuna wađanda suka bada gaskiya (sukayi Ihlasi cikin imani daga waninsu. kuma ya riƙi Shahidai daga cikinku) ya girmama su da mutuwar Shahada, Allah ba yason kafirai. (Ni'imomin dayayi musu kuwa na baƙarƙashiya ne).

1) Wato Rarshe

وَلِيُمَحِّصَ اَ۬للَّهُ اُ۬لذِينَ ءَامَنُواْ وَيَمۡحَقَ اَ۬لۡكَٰفِرِينَ ﴿141﴾ أَمۡ حَسِبۡتُمۡ
أَن تَدۡخُلُواْ اُ۬لۡجَنَّةَ وَلَمَّا يَعۡلَمِ اِ۬للَّهُ اُ۬لذِينَ جَٰهَدُواْ مِنكُمۡ
وَيَعۡلَمَ اَ۬لصَّٰبِرِينَ ﴿142﴾ وَلَقَدۡ كُنتُمۡ تَمَنَّوۡنَ اَ۬لۡمَوۡتَ
مِن قَبۡلِ أَن تَلۡقَوۡهُ فَقَدۡ رَأَيۡتُمُوهُ وَأَنتُمۡ تَنظُرُونَ ﴿143﴾
ثمن * وَمَا مُحَمَّدٌ اِلَّا رَسُولٞ قَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلِهِ اِ۬لرُّسُلُ أَفَإِيْن
مَّاتَ أَوۡ قُتِلَ اَ۪نقَلَبۡتُمۡ عَلَىٰٓ أَعۡقَٰبِكُمۡ وَمَنۡ يَنقَلِبۡ عَلَىٰ عَقِبَيۡهِ
فَلَن يَضُرَّ اَ۬للَّهَ شَيۡـٔٗا وَسَيَجۡزِے اِ۬للَّهُ اُ۬لشَّٰكِرِينَ ﴿144﴾ وَمَا كَانَ
لِنَفۡسٍ اَن تَمُوتَ إِلَّا بِإِذۡنِ اِ۬للَّهِ كِتَٰبٗا مُّؤَجَّلٗا وَمَن
يُرِدۡ ثَوَابَ اَ۬لدُّنۡيَا نُؤۡتِهِۦ مِنۡهَا وَمَن يُرِدۡ ثَوَابَ اَ۬لۡأٓخِرَةِ نُؤۡتِهِۦ
مِنۡهَا وَسَنَجۡزِے اِ۬لشَّٰكِرِينَ ﴿145﴾ وَكَأَيِّن مِّن نَّبِےٓءٖ قُتِلَ مَعَهُۥ
رِبِّيُّونَ كَثِيرٞ فَمَا وَهَنُواْ لِمَا أَصَابَهُمۡ فِے سَبِيلِ اِ۬للَّهِ
وَمَا ضَعُفُواْ وَمَا اَ۪سۡتَكَانُواْ وَاللَّهُ يُحِبُّ اُ۬لصَّٰبِرِينَ ﴿146﴾ وَمَا كَانَ
قَوۡلَهُمُۥٓ إِلَّآ أَن قَالُواْ رَبَّنَا اَ۪غۡفِرۡ لَنَا ذُنُوبَنَا وَإِسۡرَافَنَا فِےٓ أَمۡرِنَا
وَثَبِّتۡ أَقۡدَامَنَا وَانصُرۡنَا عَلَى اَ۬لۡقَوۡمِ اِ۬لۡكَٰفِرِينَ ﴿147﴾ فَـَٔاتَىٰهُمُ اُ۬للَّهُ
ثَوَابَ اَ۬لدُّنۡيَا وَحُسۡنَ ثَوَابِ اِ۬لۡأٓخِرَةِ وَاللَّهُ يُحِبُّ اُ۬لۡمُحۡسِنِينَ ﴿148﴾

141. Kuma don Allah ya tsarkake wađanda suka bada gaskiya (daga zunubai, saboda abinda yake samun su na daga wahala da mashaƙƙa,)[1] kuma donya shate kafirai.

(ZARGI GA SASHIN WANDA YA HA-LARCI DAGAR UHUDU)

142. Kai! Shin kuna zato kwa shiga Alhanna ne, har yau Allah bai nuna wađanda sukayi yaki daga cikin ku ba, kuma ya nuna masu haƙuri (a cikin tsanance - tsanance).

143. Haƙiƙa kun kasance kuna burin mutuwa tun gaban baku sadu da ita ba, (Lokacin daku ,ka ce:"Ina ma muna da rana kamar ranar Badar don mu zama mun sami darajar shahada,)" to, haƙiƙa kun ganta alhali kuna Lure (dayadda darajar shahada take, to. donme ku ka tar" watse?).

144. (Yayin da aka đaidaitacewa Annabi Sallallahu alaihi wasallama an kashe shi a cikin tar-watsewar da suka yi, munafukai sukace dasu: "In an kashe shi to ku koma addininku," sai Allah yace): Annanbi Muhammadu (Sallallahu alaihi wasallama bal kasance ba face manzo ne da mazanni suka wuce gabansa, shin to, in ya mutu ko aka kashe shi (kamar waninsa,) sai ku juya a kan dugadugan ku (a kan kafirci?) Wanda duk ya juya a kan dugaduganså, to, bazai cuci Allah komai ba, (ya cuci kansa ne kawai,) da sannu Allah zai sakawa masu godiya (da ni'imominsa da tabbata) a tagen da ga"

(ZARGIN MUMINAI DASHIRY AR DASU)

145. Bazai yiwu ga wata rai ta mutu ba sal da izinin Allah. Allah ya rubuta wannan rubutu abin iyakancewa, (ba gabata ba jinkirta, donme ku ka tarwatse? Tarwatsa bata ije mutuwa, tabbata bata kisa,) wanda yanufi sakamakon duniya da aikinsa ma bashi rabonsa daga cikinta, bashi da rabo a Lahira, wanda yanufi sakamakon lahira da aikin sa, ma bashi daga sakamakonta, Da sannu zamu sakawa masu godewa (ni'imarmu).

146. Da yawa Annabi da aka kashe shi, masana Allah masu yawa suna tare dashi, (sahabbansa, waliyyai,) to, basuji tsoro ba ga abinda ya samesu saboda Allah (na daga miyakuda kashe Annabawansu da sahabbansu,} basu karaya (ga barin yaƙi) ba, basu ƙanƙastar dakai (ga ma-gautansu) ba, (kamar daku ,ka aikata Lokacin da akace "An kashe Annabi Sallallahu alaihi wasallama)". Allah yana son masu haƙuri (a kan bala'i).

147. Wani abu bai kasance maganarsu ba (yayin kashe Annabinsu tareda tabbatar su da dauriyarsu,) sai cewarsu, "Ya Ubangijinmu! gafarta mana zunubanmu dashishshiginmu cikin al'amarinmu (sun fađi haka ne don nuna cewa wannan abu daya samesu saboda mummu-nan aikinsu ne) ka tabbatar da digadiganmu (da ƙarfi) a kan mutane kafirai!".

148. Sai Allah ya saka masu sakam-akon duniya (nasara da ganima) da kyakkyawan sakamakon Lahira (shine ya basu fiye da cancantar su,) Allah yana son masu kyautatawar aiki.

1)Wahala

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن تُطِيعُواْ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ
يَرُدُّوكُمْ عَلَىٰٓ أَعْقَٰبِكُمْ فَتَنقَلِبُواْ خَٰسِرِينَ ﴿149﴾
بَلِ ٱللَّهُ مَوْلَىٰكُمْ وَهْوَ خَيْرُ ٱلنَّٰصِرِينَ ﴿150﴾
سَنُلْقِے فِے قُلُوبِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱلرُّعْبَ
بِمَآ أَشْرَكُواْ بِاللَّهِ مَا لَمْ يُنَزِّلْ بِهِۦ سُلْطَٰناً
وَمَأْوَىٰهُمُ ٱلنَّارُ وَبِئْسَ مَثْوَى ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿151﴾
وَلَقَدْ صَدَقَكُمُ ٱللَّهُ وَعْدَهُۥٓ إِذْ تَحُسُّونَهُم بِإِذْنِهِۦ
حَتَّىٰٓ إِذَا فَشِلْتُمْ وَتَنَٰزَعْتُمْ فِے ٱلْأَمْرِ وَعَصَيْتُم
مِّنۢ بَعْدِ مَآ أَرَىٰكُم مَّا تُحِبُّونَ مِنكُم مَّن يُرِيدُ ٱلدُّنْيَا
وَمِنكُم مَّن يُرِيدُ ٱلْأٓخِرَةَ ثُمَّ صَرَفَكُمْ عَنْهُمْ لِيَبْتَلِيَكُمْ
وَلَقَدْ عَفَا عَنكُمْ وَاللَّهُ ذُو فَضْلٍ عَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿152﴾
۞ إِذْ تُصْعِدُونَ وَلَا تَلْوُۥنَ عَلَىٰٓ أَحَدٍ وَالرَّسُولُ
يَدْعُوكُمْ فِےٓ أُخْرَىٰكُمْ فَأَثَٰبَكُمْ غَمّاَۢ
بِغَمٍّ لِّكَيْلَا تَحْزَنُواْ عَلَىٰ مَا فَاتَكُمْ
وَلَا مَآ أَصَٰبَكُمْ وَاللَّهُ خَبِيرُۢ بِمَا تَعْمَلُونَ ﴿153﴾

ربع

(DAKA TA KAFIRAI DA AƘIBARSA)

149. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! m ku ka daka ta waɗanda suka kafirta (cikin abinda suke umarnin ku dashi,) sa mayar daku ,a kan digadiganku (izuwa kafirci,) ku komo taɓaɓɓu.

150. Kai! Allah ne mataimakin ku, (Allah) shine fiyayyan masu taimako.

151. Da sannu zamu jefa razani cikin zukatan waɗanda suka kafirta (bayan sun himmatu a kan komowa don tinɓuke Musuimi bayan tafiyarsu daga Uhudu, sai aka jet'a razani a zukatansu basu komo ba,) saboda sun tara da Allah abinda bai saukar da hujja (a kan bautarsa) ba, (watau gumaka.) makomarsu wuta. tir! makomar kafirai (ita!).

(ABINDA YA SAMI MUSULMI RANAR UHUDU DA SABABINSA)

152. Haƙiƙa Ubangiji yagasgata muku alƙawarinsa (daya yo muku na taimako,) yayin da kuke kashe su da izininSa ,har dai yayin da kuka firgita (ga barin yaƙi,) kuka saɓa a cikin umarnin (da Annabi ya baku na tsayuwa a gefen dutse don harbi, ba'alinku yace "Mu tafi mun ci nasara," ba 'alinku yace "A'a kada mu saɓa wa ma'aiki Sallallahu alaihi wasallama)" kuka saɓi (umarninsa kuka bar matsayin don neman ganima,) akwai daga cikin ku wanda yake son duniya (ya kau daga mat-sayinsa saboda ganima) ba yan ya nuna muku abinda kuke so na daga nasara saiya hana muku tai makon sa.Akwai daga cikinku wanda Yake son duniya, ya kau daga nat-sayinsa saboda ganima. akwai daga gareku wanda yake nufin Lahira (ya tsaya har aka kashe shi, kamar Ahdullahi Ibni Jubair yardar Allah ta tabbata a gareshi da sahabbansa,) sannan yajuyar daku, ga barin kafirai domin ya jarrabe ku (yaga mai tsarkakewa daga waninsa,) haƙiƙa yayi muku at'uwar abinda kuka aikata,) Allah mai falala ne ga muminai (da rangwame).

153.(Ka ambata) zamanin da kuke girkawa aguje ba kwa waiwayawa a kan kowa, alhali Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) yana kiranku daga bayanku yana cewa kutaho izuwa gare ni ya bayin Allahi kutahu izuwa gareni ya bayin Allah,saiya saka muku baƙin cikin (risɓawa) saboda baƙin cikinku (ga manzon Allah don kun saɓa masa sai yayi muku rangwame) don kada kuyi baƙin ciki a bisa abinda ya tsere muku (na ganima ko abin cla ya same ku na daga kisa da risɓawa,) Allah masanine da abinda kuke aikatawa.

ثُمَّ أَنزَلَ عَلَيۡكُم مِّنۢ بَعۡدِ ٱلۡغَمِّ أَمَنَةٗ نُّعَاسٗا يَغۡشَىٰ طَآئِفَةٗ مِّنكُمۡۖ
وَطَآئِفَةٞ قَدۡ أَهَمَّتۡهُمۡ أَنفُسُهُمۡ يَظُنُّونَ بِٱللَّهِ غَيۡرَ ٱلۡحَقِّ ظَنَّ
ٱلۡجَٰهِلِيَّةِۖ يَقُولُونَ هَل لَّنَا مِنَ ٱلۡأَمۡرِ مِن شَيۡءٖۗ قُلۡ إِنَّ ٱلۡأَمۡرَ
كُلَّهُۥ لِلَّهِۗ يُخۡفُونَ فِيٓ أَنفُسِهِم مَّا لَا يُبۡدُونَ لَكَۖ يَقُولُونَ لَوۡ كَانَ
لَنَا مِنَ ٱلۡأَمۡرِ شَيۡءٞ مَّا قُتِلۡنَا هَٰهُنَاۗ قُل لَّوۡ كُنتُمۡ فِي بُيُوتِكُمۡ
لَبَرَزَ ٱلَّذِينَ كُتِبَ عَلَيۡهِمُ ٱلۡقَتۡلُ إِلَىٰ مَضَاجِعِهِمۡۖ وَلِيَبۡتَلِيَ
ٱللَّهُ مَا فِي صُدُورِكُمۡ وَلِيُمَحِّصَ مَا فِي قُلُوبِكُمۡۚ وَٱللَّهُ
عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ﴿154﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ تَوَلَّوۡاْ مِنكُمۡ يَوۡمَ
ٱلۡتَقَى ٱلۡجَمۡعَانِ إِنَّمَا ٱسۡتَزَلَّهُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ بِبَعۡضِ مَا كَسَبُواْۖ
وَلَقَدۡ عَفَا ٱللَّهُ عَنۡهُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ حَلِيمٞ ﴿155﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ لَا تَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَقَالُواْ لِإِخۡوَٰنِهِمۡ إِذَا ضَرَبُواْ
فِي ٱلۡأَرۡضِ أَوۡ كَانُواْ غُزّٗى لَّوۡ كَانُواْ عِندَنَا مَا مَاتُواْ وَمَا قُتِلُواْ
لِيَجۡعَلَ ٱللَّهُ ذَٰلِكَ حَسۡرَةٗ فِي قُلُوبِهِمۡۗ وَٱللَّهُ يُحۡيِۦ وَيُمِيتُۗ
وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٞ ﴿156﴾ وَلَئِن قُتِلۡتُمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ
أَوۡ مُتُّمۡ لَمَغۡفِرَةٞ مِّنَ ٱللَّهِ وَرَحۡمَةٌ خَيۡرٞ مِّمَّا يَجۡمَعُونَ ﴿157﴾

154. Sannan ya saukar da nutsuwa a gareku bayan baƙin cikin nan, gyangyadi da yake zuwa wa wađansu jama'a daga cikinku, wađansu jama'a kuwa haƙiƙa kawukansune suka dame su (suna' ta kansu, saboda munafincinsu,) suna zato da Allah wanin gaskiya, irin zaton jahi-liyya, da suka (kuđure cewa Annabi sallAllahu alaihi wa sallama an kashe shi ko baza'a taimakeghi ba) suna cewa ba wani abu agaremu na daga tai-makon na wannan al'amari" (wai ba nasara wacce aka alƙawarta musu). Cene (dasu); "Al'amari dukkansa na Allah ne", suna ɓoyewa cikin kawu-kansu abinda basa bayyanawa gareka, (watau shine fadinsu; "Da wani abu ya kasance garemu na daga wannan Lamari, da ba a kashe mu a nan ba)". cene (dasu); "Da kun kasance a cikin daƙunanku (ya zama a cikinku akwai wanda Allah ya rubuta masa kisa) da wađanda aka rubuta musu kisan nan a kansu, dasun fito izuwa wurin fađuwarsu, (a kashe su, gudun ƙaddara guzurin tarar da ita ne", an aikata abinda aka aikata a Uhudu) don Allah yajarrabi abinda yake cikin zukatanku, (na Ihlasi da nifaƙa) kuma don rarrabe abinda yake cikin zukatanku, Allah masanine da abinda yake cikin zukata.

155. Haƙiƙa wađannan da sukajuya baya daga gareku (ga barin yaƙi) ranar da runduna biyu ta hađu (Musulami da kafirai,) shaiđan ya kau dasune (,da wasuwasinsa kawai.) saboda ba'alin abinda suka tsuwurwuta (na zunubi shine saba wa umarnin Annabi Sallallahu alaihi wasallama), haƙiƙa Allah yayi atuwa ga barinsu, Allah mai ga-fara ne mai jinkirin azaba.

(ZABURAR UA MUTANE A KAN YAƘI DA RASHIN TSORON MUTUWA)

156. Yaku wađanda suka bada gadkiya kadaku ,zamo kamar wađannan da suka kafirta (watau munafuƙai) suka fađa (a cikin sha'anin) "yan"uwansu, yayin da sukayi tafiya a cikin ƙasa (suka mutu ko suka kasance mayaƙa aka kashe su,) "dasun ƙasance a wurinmu da basu mutu ba. kuma da ba a kashe su ba, "don Allah yasanya wancananka (magana a karshen al'amari) nadama a cikin zukatansu. Allah ne yake rayawu, yake malarwa, (ɓuyabaya hana inutuwa,) Allah masanine da abinda kuke aikatawa.

157. Wallahi idan an kashe ku (a cikin yaƙi) koku ka miuu (a gida) Lallai gafara daga Allah da jinƙai shi yafi daga abindaku ,ke tarawa (na duniya).

وَلَئِن مُّتُّمۡ أَوۡ قُتِلۡتُمۡ لَإِلَى ٱللَّهِ تُحۡشَرُونَ ﴿158﴾ فَبِمَا رَحۡمَةٍ مِّنَ ٱللَّهِ
لِنتَ لَهُمۡۖ وَلَوۡ كُنتَ فَظًّا غَلِيظَ ٱلۡقَلۡبِ لَٱنفَضُّواْ مِنۡ حَوۡلِكَۖ
فَٱعۡفُ عَنۡهُمۡ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لَهُمۡ وَشَاوِرۡهُمۡ فِي ٱلۡأَمۡرِۖ فَإِذَا عَزَمۡتَ
فَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُتَوَكِّلِينَ ﴿159﴾ * إِن يَنصُرۡكُمُ ٱللَّهُ ثمن
فَلَا غَالِبَ لَكُمۡۖ وَإِن يَخۡذُلۡكُمۡ فَمَن ذَا ٱلَّذِي يَنصُرُكُم
مِّنۢ بَعۡدِهِۦۗ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ﴿160﴾ وَمَا كَانَ لِنَبِيٍّ
أَن يَغُلَّۚ وَمَن يَغۡلُلۡ يَأۡتِ بِمَا غَلَّ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۚ ثُمَّ تُوَفَّىٰ كُلُّ
نَفۡسٍ مَّا كَسَبَتۡ وَهُمۡ لَا يُظۡلَمُونَ ﴿161﴾ أَفَمَنِ ٱتَّبَعَ رِضۡوَٰنَ ٱللَّهِ
كَمَنۢ بَآءَ بِسَخَطٍ مِّنَ ٱللَّهِ وَمَأۡوَىٰهُ جَهَنَّمُۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ﴿162﴾
هُمۡ دَرَجَٰتٌ عِندَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ بَصِيرُۢ بِمَا يَعۡمَلُونَ ﴿163﴾ لَقَدۡ مَنَّ ٱللَّهُ
عَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ إِذۡ بَعَثَ فِيهِمۡ رَسُولًا مِّنۡ أَنفُسِهِمۡ يَتۡلُواْ
عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتِهِۦ وَيُزَكِّيهِمۡ وَيُعَلِّمُهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ
وَإِن كَانُواْ مِن قَبۡلُ لَفِي ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿164﴾ أَوَلَمَّآ أَصَٰبَتۡكُم
مُّصِيبَةٌ قَدۡ أَصَبۡتُم مِّثۡلَيۡهَا قُلۡتُمۡ أَنَّىٰ هَٰذَاۖ قُلۡ هُوَ مِنۡ
عِندِ أَنفُسِكُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ﴿165﴾

158. Wallahi idan kun muto ko aka kashe ku a yaƙi, haƙiƙa izuwa Allah za a tara ku.

(BA'ALIN TA'DODINSA SALLALAHU ALAHI WASALLAMA)

159. Saboda dai rahama daga Allah ne kawai; kayi taushi garesu. (Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama zamanin da suka suɓa umaminka) daka kasance mai mummunan hali, mai kaushin zuciya, da saisu tarwatse daga daura da kai, sai kayi rangwame ga barinsu, ka nema musu gafara (daga zunubansui ka shawarce su cikin Lamarinka (na yaƙi ko waninsa, don daɗaɗawa ga zukatansu don kuma ai koyi da kai, saboda haka yake yawan shawartarsu, Sallallahu alaihi wasallama,) to, idan kai ƙudurin aniya (a bisa zartada al'amarin daka nufa bayan shawara,) to ka dogara ga Allah (bada shawarar ba,) haƙiƙa Ubangiji yana son masu dogara a gareshi.

160. In Ubangiji ya taimake ku (a kan magauta, kamar ranar Badar,) to, ba mai rinjaye a kanku, in kuma bai baku nasara ba (kamar ranar Uhudu)to, wanene wandazai taimake ku bashi ba? Muminai su dogara ga Allah shi kaɗai.

(HARAMCIN GULULU WATAU HA'INCI, DA WANI ABU DAGA SU-FOHNSA SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

161. Bai kamata ga Annabi yayi ha'inci a cikin ganima ba, wanda duk yayi ha'inci zal zoda abin daya ha'inta ranar Alƙiyama (yana dauƙe dashi a kan wuyansa,} sannan a cikawa kowace rai abindata aikata, kuma.su, baza a zalunce su komai ba.

162. Yanzu wanda yabi yardar Allah, zai zama kamar wanda yakomo da fushi na Allah? Makomarsa Jahannanma, tir! Makoma (ita').

163. Su (ma'abuta) darajoji ne gun Allah, Allah masanine da abinda suke aikatawa.

164. Haƙiƙa Allah yayi baiwa bisa muminai daya aiko manzo a cikinsu daga kawunansu, balarabe donsu fahimta daga - gare ghi su ɗaukakaka saboda shi, ba mala'ika baba baubawa ba. yana karanta ayoyinsa a garesu, (Alƙur'ani) yana tsarkake su (daga zunubai) yana sanar dasu Alƙur'ani (watau yanayi musu tafsirinsa) da hikima (hadisi), haƙiƙa su sun kasance gaban aiko shi. Lallai suna cikin ɓata mabayyani.

(BA'ALIN MIYAGUN AIKIN YAHUDAWA)

165. Ashe yayin da musibata same ku (da kashe mutum saba'in naku a ranar Uhudu,) alhali kun sami ninkinta biyu (a badar da kashe mutum saba'in da ribace mutun saba'in nasu,} sai ku ce "Ta ina wannan faɗuwa ta same mu (ga mu Musulmi ga manzon Allah a cikmmu?) Cene (dasu) "Shi (wannan taɓewa) daga kawukanku ne, (don kun bar wurin tsayawa da aka umarce kuda tsayuwa a cikinsa,) haƙiƙa Ubangiji mai iko ne bisa komai".

وما أصابكم يوم التقى الجمعان فبإذن الله وليعلم المؤمنين ﴿166﴾
وليعلم الذين نافقوا وقيل لهم تعالوا قاتلوا في سبيل الله
أو ادفعوا قالوا لو نعلم قتالا لاتبعناكم هم للكفر
يومئذ أقرب منهم للإيمان يقولون بأفواههم ما ليس
في قلوبهم والله أعلم بما يكتمون ﴿167﴾ الذين قالوا لإخوانهم
وقعدوا لو أطاعونا ما قتلوا قل فادرءوا عن أنفسكم
الموت إن كنتم صادقين ﴿168﴾ ولا تحسبن الذين قتلوا
في سبيل الله أمواتا بل أحياء عند ربهم يرزقون ﴿169﴾
فرحين بما آتاهم الله من فضله ويستبشرون بالذين
لم يلحقوا بهم من خلفهم ألا خوف عليهم ولا هم
يحزنون ﴿170﴾ * يستبشرون بنعمة من الله وفضل وأن الله
لا يضيع أجر المؤمنين ﴿171﴾ الذين استجابوا لله والرسول من
بعد ما أصابهم القرح للذين أحسنوا منهم واتقوا أجر
عظيم ﴿172﴾ الذين قال لهم الناس إن الناس قد جمعوا لكم فاخشوهم
فزادهم إيمانا وقالوا حسبنا الله ونعم الوكيل ﴿173﴾

حزب

166. Abinda ya same ku ranar da runduna guda hiyu ta haɗu (a uhudu) to, da nufin Allah ne kuma don Ubangiji ya nuna muminai (na gaskiya).
167. Kuma donya nuna waɗanda sukayi munafunci, waɗanda akace dasu; "Kuzo kuyi yaƙi saboda Allah. (abdullahi ke nan ɗan Ubayyu da abokansa) koku ije mana (mutane da yawan jama'arku in baku sami damar yaƙi ba,)' saisu ce: "Da mun iya yaki da mun bi ku". (Ubangiji ya faɗa don ƙaryatawa garesu,) "su ga kafirci a wannan rana mafi kusanci ne daga su. izuwa imani, suna faɗa da bakunansua"[1] abinda baya cikin zukatansu, Allah masanine da abinda suke ɓoyewa (na daga munafunci)".
168. (Su ne) waɗanda suka faɗa ga "yan'uwansu (na addini) alhali sun zauna (ga barin yaƙi); "Dasun bi mu da ba a kashe su ba," Cene (dasu): "ku ije mutuwa ga barin kanku m kun kasanee magasganta (a cikin cewa zama yana tserarwa ga mutuwa)".

(SHAHIDAI DA MAYAƘA SABODA ALLAH DA SAKAMAKONSU)

169. Kadaka zaci waɗanda aka kashe su a cikin inganta Addinin Allah matattu ne bari' su; rayayyu ne nan ga Ubangijinsu, ra yukansu suna cikin maro ron tsuntsaye korra tana kiwo cikin aljanna indata ga dama tamfar da hadisi yazoda haka.Ana azurta su.
170. Masu farin ciki da abinda Allah ya basu daga falalarsa. su masu farin ciki ne da waɗanda basu risku dasu bana bayansu. (suna cewa): "Ba tsoro a garesu (a duniya) baza suyi bakin ciki (a Lahira) ba".
171. Suna farin ciki da sakamako daga Allah da kari a kansa, kuma haƙiƙa Allah baya tozarta Ladan mumina.
172. Waɗanda suka amsa ga Allah da ma'aikin Allah (da fita yaki yayin da Abu Sufuyana da abokansa suka nufi komawa sukai alƙawarin kasuwar Badar tareda manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama shekara mai gabatowa ranar Uhudu) bayan miki ya samesu a Uhudu, Lada mai girma ya tabbata ga waɗanda sukayi kyakkyawan aiki daga garesu, sukaji tsoron (saɓa masa).
173. Waɗanda mutane sukace dasu wato (Nu'aimu dan Masa'udu gaban musuluncinsa) Haƙiƙa mutane (Abu - Sufyana da mu-tanensa) haƙiƙa sun tara (runduna) don ku, (donsu tunɓuke ku,) kuji tsoronsu" sai (wannan faɗa) ta ƙara musu ban gaskiya (da Allah da sakankancewa dashi,) suka ce: "Allah ne mai isar mana (Lamarinsu,) madalla abin dogaro (Ubangiji)".

1) Shine da mun iya yaƙi da mun bika

فَانقَلَبُواْ بِنِعۡمَةٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَفَضۡلٖ لَّمۡ يَمۡسَسۡهُمۡ سُوٓءٞ
وَاتَّبَعُواْ رِضۡوَانَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ ذُو فَضۡلٍ عَظِيمٍ ﴿174﴾ إِنَّمَا ذَٰلِكُمُ
ٱلشَّيۡطَٰنُ يُخَوِّفُ أَوۡلِيَآءَهُۥ فَلَا تَخَافُوهُمۡ وَخَافُونِ إِن كُنتُم
مُّؤۡمِنِينَ ﴿175﴾ وَلَا يَحۡزُنكَ ٱلَّذِينَ يُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡكُفۡرِۚ إِنَّهُمۡ لَن يَضُرُّواْ ٱللَّهَ
شَيۡـٔٗاۚ يُرِيدُ ٱللَّهُ أَلَّا يَجۡعَلَ لَهُمۡ حَظّٗا فِي ٱلۡأٓخِرَةِۖ وَلَهُمۡ عَذَابٌ
عَظِيمٌ ﴿176﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱشۡتَرَوُاْ ٱلۡكُفۡرَ بِٱلۡإِيمَٰنِ لَن يَضُرُّواْ ٱللَّهَ
شَيۡـٔٗاۖ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ﴿177﴾ وَلَا يَحۡسَبَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَنَّمَا
نُمۡلِي لَهُمۡ خَيۡرٞ لِّأَنفُسِهِمۡۚ إِنَّمَا نُمۡلِي لَهُمۡ لِيَزۡدَادُوٓاْ إِثۡمٗاۖ وَلَهُمۡ
عَذَابٞ مُّهِينٞ ﴿178﴾ * مَّا كَانَ ٱللَّهُ لِيَذَرَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ عَلَىٰ مَآ أَنتُمۡ عَلَيۡهِ
حَتَّىٰ يَمِيزَ ٱلۡخَبِيثَ مِنَ ٱلطَّيِّبِۗ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُطۡلِعَكُمۡ عَلَى ٱلۡغَيۡبِ
وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَجۡتَبِي مِن رُّسُلِهِۦ مَن يَشَآءُۖ فَـَٔامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦۚ
وَإِن تُؤۡمِنُواْ وَتَتَّقُواْ فَلَكُمۡ أَجۡرٌ عَظِيمٞ ﴿179﴾ وَلَا يَحۡسَبَنَّ
ٱلَّذِينَ يَبۡخَلُونَ بِمَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦ هُوَ خَيۡرٗا لَّهُمۖ
بَلۡ هُوَ شَرّٞ لَّهُمۡۖ سَيُطَوَّقُونَ مَا بَخِلُواْ بِهِۦ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ
وَلِلَّهِ مِيرَٰثُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٞ ﴿180﴾

ثمن

174. Sai suka koma (daga badar) da sakamako daga Allah da ƙari (a kansa) suka koma sumul tareda riba, wani abu mummuna bai samesu ba; (kisa ko miki,) suka bi yardar Allah (da ma'aikinsa a cikin fita,) Allah mai falala ne maigirma (ga masu biyayya ga reshi).

175. Wancananku (mai cewa "INNAN NASA.") [1] Shaiɗan ne kawai yake tsoratar daku ,waliyansa (kafirai) to, kadaku ,ji tsoron su, kuji tsorona in kun kasance muminai (na gaskiya).

(TALALA MAI KAMAR SAKE DA) (RARRASHIN ANNABI "SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA" DA BAYANIN BA'ALIN HUKUNCI)

176. Kada waɗannan dasuke gaggawa a cikin kafirci su baƙan tamaka, haƙiƙa su bazasu cuci Allah da komai ba (da aikinsu,) Allah yana nutin bazai basu rabo a Lahira ba (aljanna,) azaba maigirma ta tabbata garesu (a cikin wuta).

177. Haƙiƙa waɗanda suka sayi kat"irci da imani bazasu cuci Allah da komai ba, azaba mai raɗaɗi na guresu.

178. Kada waɗanda suka kafirta su zaci jinkirin da muke musu alhairi ne ga kawukansu, munayi musujinkiri ne kawai da tsawaita ra yu kan su da jinkir ta musu azaba donsu ƙara zunubi. azaba mai wulakantarwa na garesu.

179. Allah bazai bar muminai a kan abindaku ,ke kansa ba, (na cuɗanyar mai gaskiya da waninsa) saiya rarrabe munafuki daga mumini, Allah bai kasance ya tsinkayar daku ,a kan gaibu ba, sai dai Ubangiji yana zaɓin wanda yaga dama daga man-zanninsa, (saiya tsinkayar dashi gaibu tamkar daya tsinkayar da Annabi Sallallahu alaihi wasallama bisa halin munafukai). To, ku bada gaskiya da Allah da manzanninsa, in kun bada gaskiYaku kaji tsoron Allah to, Lada maigirma yana gareku.

(ROWA DA (ƘARYA DA SAKAMAKONSU)

180. Kadaka zaci waɗannan dasuke rowa da abinda Allah ya basu na daga falalarsa, (suna hana Zakka ko kyauta) ita rowar nan alhairi ce garesu, (ba alhairi ce ba,) bari! ita sharri ce garesu, Da sannu za a rataya musu abinda sukayi rowar nan dashi (a wuya) ranar Alƙiyama, (ya zama micijiya a wuyansu tana saransu, tamfar dayazo cikin hadisi,) gadon sammai da ƙassaina Allah ne (zai gaje su bayan karewar mazaunansu,) Allah macikin sanine da abinda suke aikatawa.

1)WaloNu'aimu

لَقَدْ سَمِعَ اَ۬للَّهُ قَوْلَ اَ۬لَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّ اَ۬للَّهَ فَقِيرٞ وَنَحْنُ
أَغْنِيَآءُۖ سَنَكْتُبُ مَا قَالُواْ وَقَتْلَهُمُ اُ۬لَانۢبِيٓـَٔاءَ بِغَيْرِ حَقّٖ
وَنَقُولُ ذُوقُواْ عَذَابَ اَ۬لْحَرِيقِۖ (181) ذَٰلِكَ بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيكُمْ
وَأَنَّ اَ۬للَّهَ لَيْسَ بِظَلَّٰمٖ لِّلْعَبِيدِۖ (182) اِ۬لَّذِينَ قَالُوٓاْ
إِنَّ اَ۬للَّهَ عَهِدَ إِلَيْنَآ أَلَّا نُؤْمِنَ لِرَسُولٍ حَتَّىٰ يَأْتِيَنَا
بِقُرْبَانٖ تَأْكُلُهُ اُ۬لنَّارُۖ قُلْ قَدْ جَآءَكُمْ رُسُلٞ مِّن قَبْلِے
بِالْبَيِّنَٰتِ وَبِالذِے قُلْتُمْ فَلِمَ قَتَلْتُمُوهُمْ إِن كُنتُمْ
صَٰدِقِينَۖ (183) فَإِن كَذَّبُوكَ فَقَدْ كُذِّبَ رُسُلٞ مِّن قَبْلِكَ
جَآءُو بِالْبَيِّنَٰتِ وَالزُّبُرِ وَالْكِتَٰبِ اِ۬لْمُنِيرِۖ (184) كُلُّ نَفْسٖ
ذَآئِقَةُ اُ۬لْمَوْتِۖ وَإِنَّمَا تُوَفَّوْنَ أُجُورَكُمْ يَوْمَ اَ۬لْقِيَٰمَةِۖ
فَمَن زُحْزِحَ عَنِ اِ۬لنَّارِ وَأُدْخِلَ اَ۬لْجَنَّةَ فَقَدْ فَازَۖ
وَمَا اَ۬لْحَيَوٰةُ اُ۬لدُّنْيَآ إِلَّا مَتَٰعُ اُ۬لْغُرُورِۖ (185) * لَتُبْلَوُنَّ فِےٓ أَمْوَٰلِكُمْ
وَأَنفُسِكُمْ وَلَتَسْمَعُنَّ مِنَ اَ۬لَّذِينَ أُوتُواْ اُ۬لْكِتَٰبَ
مِن قَبْلِكُمْ وَمِنَ اَ۬لَّذِينَ أَشْرَكُوٓاْ أَذٗى كَثِيراٗۖ
وَإِن تَصْبِرُواْ وَتَتَّقُواْ فَإِنَّ ذَٰلِكَ مِنْ عَزْمِ اِ۬لْأُمُورِۖ (186)

ربع

181. Hakika Ubangiji yaji fadin wadanda Sukace, " hakika Allah mabukaci ne, mu mawadata ne", (sune Yahudu. sun fadi wannan zamanin da Ubangiji ya saukar da "Waye zai ranta wa Allah rance kyakkyawa?" Sukace "Da mawadaci ne da bai nemi rance gun mu ba"). Dasunnu zamu saka musu abinda -suka fada da kisan su Annabawa bada gaskiya ba, muna cewa dasu (a harshen Mala'iku) ku dandani azabar wuta.

182. "Wancananka (azaba) saboda abinda hannuwanku ta gabatar ne, kuma hakika Ubangiji ba mai zalintar bayi ne ba".

183. (Su ne) wadanda sukace da Annabi Sallallahu alaihi wasallama) " hakika Ubangiji ya alkawarta izuwa garemu (a cikin Attaura,) kada mu bada gaskiya dan wani manzo, sai yazo mana da hadaya wacce wuta zata ci shi," Cene: (dasu don kurustawa "hakik.a manzanni a gabana sun zo mukuda mu'ujuzozi da kuma abindaku ,ka fada, (kamar Annabi Zakariya, da yahaya tsiran Allah ya tabbata a garesu, ku ka kashe su, watau Yahudu na zamanin Annabi ake nufi,) to, donme ku ka kashe su in kun kasance magasgata?".

184. In sun ki gasgata ka, to, hakika an karyata manzannl gabam ka, sun zoda mu'ujuzozi da Littattafai, (kamar na Annabi Ibrahimu) da Littafi mai haske, (kamar Attaura da Injila, to, sai ka daure tamfar da suka daure).

KARSHEN KOWANE MAI RAI MU TUWA DUK KAN MAI RAI ZAI MUTU NE

185. Dukkan rai mai dandanar mutuwa ce. Dahir dai ana cika muku Ladanku ranar Alkiyama ne. wanda aka nisan tashi ga harin wuta aka shigar dashi Al-janna, to, hakik.a ya rabauta. Rayuwar duniyabata kasance ba sai amfanin rudi (a ji dadi dashi kadan sannan ya kare).

186. Lallai za a a jarrabe ku a cikin dukiyoyinku, (da fitar da farillai a cikinta, wato karayar damuna) da kuma cikin kawukanku (da ibadu da jarrabu). Lallai zakuji cuta mai yawa daga wadanda aka basu Littafi gabanku (Yahudu da Nasara). Kuma daga wadanda suke mushirkan Larabawa (zakuji zagi da cin mutunci,) idan ku ka daure (a bisa wannan) ku kaji tsoron Allah to, hakika wancanenka yana daga matsananta al'amura (wajibai).

(SASHIN MIYAGUN HALAYEN AHLUL - KITABI) YA HUDU DA NASARA DA "YA" YANSU AMERIKA

وَإِذْ أَخَذَ اللَّهُ مِيثَاقَ الَّذِينَ أُوتُوا الْكِتَابَ لَتُبَيِّنُنَّهُ
لِلنَّاسِ وَلَا تَكْتُمُونَهُ فَنَبَذُوهُ وَرَاءَ ظُهُورِهِمْ وَاشْتَرَوْا
بِهِ ثَمَنًا قَلِيلًا فَبِئْسَ مَا يَشْتَرُونَ ﴿187﴾ لَا تَحْسَبَنَّ
الَّذِينَ يَفْرَحُونَ بِمَا أَتَوا وَيُحِبُّونَ أَنْ يُحْمَدُوا بِمَا لَمْ يَفْعَلُوا
فَلَا تَحْسَبَنَّهُمْ بِمَفَازَةٍ مِنَ الْعَذَابِ وَلَهُمْ عَذَابٌ
أَلِيمٌ ﴿188﴾ وَلِلَّهِ مُلْكُ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ وَاللَّهُ
عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ﴿189﴾ إِنَّ فِي خَلْقِ السَّمَاوَاتِ
وَالْأَرْضِ وَاخْتِلَافِ اللَّيْلِ وَالنَّهَارِ لَآيَاتٍ لِأُولِي الْأَلْبَابِ ﴿190﴾
الَّذِينَ يَذْكُرُونَ اللَّهَ قِيَامًا وَقُعُودًا وَعَلَىٰ جُنُوبِهِمْ وَيَتَفَكَّرُونَ
فِي خَلْقِ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ رَبَّنَا مَا خَلَقْتَ هَٰذَا بَاطِلًا سُبْحَانَكَ
فَقِنَا عَذَابَ النَّارِ ﴿191﴾ رَبَّنَا إِنَّكَ مَنْ تُدْخِلِ النَّارَ فَقَدْ أَخْزَيْتَهُ
وَمَا لِلظَّالِمِينَ مِنْ أَنْصَارٍ ﴿192﴾ رَبَّنَا إِنَّنَا سَمِعْنَا مُنَادِيًا يُنَادِي
لِلْإِيمَانِ أَنْ آمِنُوا بِرَبِّكُمْ فَآمَنَّا رَبَّنَا فَاغْفِرْ لَنَا ذُنُوبَنَا وَكَفِّرْ
عَنَّا سَيِّئَاتِنَا وَتَوَفَّنَا مَعَ الْأَبْرَارِ ﴿193﴾ رَبَّنَا وَآتِنَا مَا وَعَدْتَنَا عَلَىٰ
رُسُلِكَ وَلَا تُخْزِنَا يَوْمَ الْقِيَامَةِ إِنَّكَ لَا تُخْلِفُ الْمِيعَادَ ﴿194﴾

187. (Ka ambata) zamanin da Allah ya riƙi alƙawarin waɗanda aka basu Littafi, (a cikin Attaura) Lallai zaku bayyana shi ga mutane bazaku ɓoye shi ba, sai suka jefar dashi bayan - bayansu, suka sayi ɗan tamani kaɗan maimakon sa. to, wannan ciniki nasu ya mugusta'.

188. kada waɗanda suke farin ciki da abinda suka aikata (,na daga ɓatar da mutane) suke kuma son a yabe su da abinda basu aika-ta ba, to, kadasu zaci sun tsira daga azabar Ubangijr. kadaka zace su matsera daga azaba azaba mai radadi (ta tabbata; garesu).

189. Mulkin sammai da ƙassaina g Allah (taskokin ruwa da tsiri da waninsa) Allah ne mai iko bisa; komai. (,yana daga gareshi azabtar da kafirai da tserantar da muminai).

(ZIKIRIN ALLAH DA TUNANI A CIKIN HALITTARSA DA AMFANINSU)

190. Haƙiƙa akwai ayoyi (masu nuna girman Allah) a cikin ha" littar sainmai da ƙassai (da abinda ke cikinsu na mana kai,) dakai - kawon dare da rana; (ta wajen zuwa da komowa da ƙari da daɗi) ga ina'abutan hankula.

191. Waɗanda suke ambaton Allah a tsaye da zaune da kishingiɗe, (a kowane hali), suke tunani a cikin halittar sammai da ƙassai, (suna cewa): "ya Ubangijinmu! baka halicci wannan don wasa ba (sai donya shiryar a kan girman ikonka,) Tsarki ya tabbata gareka (ga barin wasa,) ka kiyashe mu azabar wuta.

192. "Ya Ubangijinmu! haƙiƙa kai wandaka shigar dashi wuta, (donya dauwama a cikinta) haƙiƙ.a ka kunyata shi. kafurai basu da masu hana masu azabar Allah.

193. "Ya Ubangijinmu! haƙiƙa Munji mai kira izuwa imani, (shine Annabi Sallallahu alaihi wasalLama" cewa ku bada gaskiya da Ubangijinku, to, muka gasgata dashi. Ya Ubangijinmu! gafarta mana zunubanmu, ka kankare mana miyagun ayyaukanmu, ka karɓi ranmu tareda managarta (Annabawa da salihai).

194. "Ya Ubangijinmu' bamu abinda ka alƙawarta mana a kan (harshen) manzanmnka, (na daga rahama da falala, ka sanya mu macanantansa,) kadaka kunyatamu ranar Alƙiyama. Haƙiƙa kai baka saɓa alƙawari".

ثمن

* فَاسْتَجَابَ لَهُمْ رَبُّهُمْ أَنِّي لَا أُضِيعُ عَمَلَ عَامِلٍ مِّنكُم
مِّن ذَكَرٍ أَوْ أُنثَىٰ بَعْضُكُم مِّنۢ بَعْضٍ فَالَّذِينَ هَاجَرُوا
وَأُخْرِجُوا مِن دِيَارِهِمْ وَأُوذُوا فِي سَبِيلِي وَقَٰتَلُوا
وَقُتِلُوا لَأُكَفِّرَنَّ عَنْهُمْ سَيِّئَاتِهِمْ وَلَأُدْخِلَنَّهُمْ
جَنَّاتٍ تَجْرِي مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَارُ ثَوَابًا مِّنْ عِندِ اللَّهِ
وَاللَّهُ عِندَهُ حُسْنُ الثَّوَابِ ﴿195﴾ لَا يَغُرَّنَّكَ تَقَلُّبُ
الَّذِينَ كَفَرُوا فِي الْبِلَادِ ﴿196﴾ مَتَاعٌ قَلِيلٌ
ثُمَّ مَأْوَاهُمْ جَهَنَّمُ وَبِئْسَ الْمِهَادُ ﴿197﴾
لَٰكِنِ الَّذِينَ اتَّقَوْا رَبَّهُمْ لَهُمْ جَنَّاتٌ تَجْرِي
مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَارُ خَالِدِينَ فِيهَا نُزُلًا مِّنْ عِندِ اللَّهِ
وَمَا عِندَ اللَّهِ خَيْرٌ لِّلْأَبْرَارِ ﴿198﴾ وَإِنَّ مِنْ أَهْلِ
الْكِتَابِ لَمَن يُؤْمِنُ بِاللَّهِ وَمَا أُنزِلَ إِلَيْكُمْ وَمَا أُنزِلَ
إِلَيْهِمْ خَاشِعِينَ لِلَّهِ لَا يَشْتَرُونَ بِآيَاتِ اللَّهِ ثَمَنًا قَلِيلًا
أُولَٰئِكَ لَهُمْ أَجْرُهُمْ عِندَ رَبِّهِمْ إِنَّ اللَّهَ سَرِيعُ الْحِسَابِ ﴿199﴾ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ
آمَنُوا اصْبِرُوا وَصَابِرُوا وَرَابِطُوا وَاتَّقُوا اللَّهَ لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿200﴾

195. Sai Ubangijinsu ya amsa musu (rokonsu,) " haƙiƙa ni bana tozarta aikin mai aiki daga gareku, namiji ko mace, "ba'alinku daga ba'ali yake. (Yayin da Ummu - Salmata Tace "Ni ban ji ana ambaton matada komai ba a cikin sha'anin hijira" sai Allah yace); "To waɗannan da sukayi hijira (daga Makka izuwa Madina) aka fusshe su daga gidaddajinsu. aka cuce su a cikin addinina, suka yaƙi (kafirai,) aka kashe su, Lallai zan kankare musu miyagun ayyukansu ga buransu, (in yi musu gafara) Lallai zan shigar dasu aljannatai da ƙoramu suke kwarara ƙarƙashinta don sakamako daga Allah, Allah kyakkyawan sakamako yana gareshi".

(HANI GA BL'RAN RUDUWA DA JIN DADIN KAFIRAI A DUNIYA)

196. (Yayin da musulmi suka ce. "kafirai suna cikin jm daɗi mu ko muna cikin wahala," sai Allah yace): "Kada wadakar hafi" rai a cikin garuruwa ta ruɗe kn (ta wajen ciniki da barazana da mulkin mallaka da karfafe - kar-fafen banza).

197. "Dan amfanine kaɗan (mai ƙarewa sannan makomarsu Ja-hannamna, tir! dashimfida (ita)".

198. Sai dai waɗannan da sukaji tsoron Ubangijinsu atjannatai na garesu da ƙoramu take kwarara ƙarƙashinta. masu dauwama a cikinta garar baƙi daga Ubangiji. abinda yake wurin Ubangiji shl yafi amfani ga managarta.

199. Haƙiƙa akwai daga mazowa Littafi wanda ya bada gaskiya da Allah, (kamar Abdullahi bini Salam da Najashi da abokansu) da abinda aka saukar a gareku (na Alkur'ani,) da abinda aka saukar garesu (na Attaura da Linjila,) suna masu ƙanƙan da dakai ga Allah, basa musanyo dan tamani ƙanƙanni maimakon ayoyin Allah, (na duniya). Waɗancananka Ladansu na garesu wurin Ubangijinsu, (za a basu shi sau biyu tamfar na cikin Suratul ƙasasi). Haƙiƙa Ubangiji mai gaggawar sakamako ne (zaiyi wa halitta hisabi a cikin gwargwadon rabin wuni na daga kwanikan duniya),

200. Ya waɗanda suka bada gaskiya! ku daure (a kan da'o'i da masifu da barin saɓo) ku rinjayi kafirai a cikin haƙuri, kuyi zaman dirshan a kan jihadi. kuji tsoron Allah (a cikin dukan haluluwanku) don ku rabauta (da Aljanna ku tsira daga wuta).

4 سُورَةُ النِّسَآءِ مَدَنِيَّة

وَهِيَ مِائَةٌ وَخَمْسٌ وَسَبْعُونَ ءَايَةً 175

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا النَّاسُ اتَّقُواْ رَبَّكُمُ الَّذِے خَلَقَكُم مِّن نَّفْسٍ وَٰحِدَةٍ وَخَلَقَ مِنْهَا زَوْجَهَا
وَبَثَّ مِنْهُمَا رِجَالًا كَثِيرًا وَنِسَآءً وَاتَّقُواْ اللَّهَ الَّذِے تَسَّآءَلُونَ بِهِۦ وَالْأَرْحَامَ
إِنَّ اللَّهَ كَانَ عَلَيْكُمْ رَقِيبًا ﴿1﴾ وَءَاتُواْ الْيَتَٰمَىٰٓ أَمْوَٰلَهُمْ وَلَا تَتَبَدَّلُواْ الْخَبِيثَ بِالطَّيِّبِ
وَلَا تَأْكُلُوٓاْ أَمْوَٰلَهُمْ إِلَىٰٓ أَمْوَٰلِكُمْ إِنَّهُۥ كَانَ حُوبًا كَبِيرًا ﴿2﴾ وَإِنْ خِفْتُمْ أَلَّا تُقْسِطُواْ
فِے الْيَتَٰمَىٰ فَانكِحُواْ مَا طَابَ لَكُم مِّنَ النِّسَآءِ مَثْنَىٰ وَثُلَٰثَ وَرُبَٰعَ فَإِنْ خِفْتُمْ
أَلَّا تَعْدِلُواْ فَوَٰحِدَةً أَوْ مَا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُكُمْ ذَٰلِكَ أَدْنَىٰٓ أَلَّا تَعُولُواْ ﴿3﴾ وَءَاتُواْ
النِّسَآءَ صَدُقَٰتِهِنَّ نِحْلَةً فَإِن طِبْنَ لَكُمْ عَن شَےْءٍ مِّنْهُ نَفْسًا فَكُلُوهُ هَنِيٓـًٔا
مَّرِيٓـًٔا ﴿4﴾ وَلَا تُؤْتُواْ السُّفَهَآءَ أَمْوَٰلَكُمُ الَّتِے جَعَلَ اللَّهُ لَكُمْ قِيَٰمًا وَارْزُقُوهُمْ فِيهَا
وَاكْسُوهُمْ وَقُولُواْ لَهُمْ قَوْلًا مَّعْرُوفًا ﴿5﴾ * وَابْتَلُواْ الْيَتَٰمَىٰ حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغُواْ (ربع)
النِّكَاحَ فَإِنْ ءَانَسْتُم مِّنْهُمْ رُشْدًا فَادْفَعُوٓاْ إِلَيْهِمْ أَمْوَٰلَهُمْ وَلَا تَأْكُلُوهَآ
إِسْرَافًا وَبِدَارًا أَن يَكْبَرُواْ وَمَن كَانَ غَنِيًّا فَلْيَسْتَعْفِفْ وَمَن كَانَ فَقِيرًا
فَلْيَأْكُلْ بِالْمَعْرُوفِ فَإِذَا دَفَعْتُمْ إِلَيْهِمْ أَمْوَٰلَهُمْ فَأَشْهِدُواْ عَلَيْهِمْ وَكَفَىٰ بِاللَّهِ حَسِيبًا ﴿6﴾

Suratun Nisa'i

An Saukar Da Ita A Madina Ayoyinla (ɗari Da Saba'in Da Biyar (175)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, Mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe

GAMUWAR MUTANE A CIKIN ASALI DAYA ANNABI ADAMU ALAIHIS-SALAMU BA BIRI BA NE)

1. Yaku mutane! kuji tsoron Ubangijinku, wanda ya halicce ku daga kai guda ɗaya (Annabi Adamu, ya halicci matarsa daga gareshi, Hauwa'u daga wani kashi daga ƙasusuwan haƙurƙuransa na hagun,) mataye (daga garesu). Kuji tsoron Allah wanda kuke magiya dashi (a tsakaninku,) kuji tsoron zumunta (karku ɓata ta,) haƙiƙa Ubangiji ya tabbata mai la'akari a kanku.

(MARAYU DA MU'AMALA DASU A CIKIN DUKIYOYINSU)

2. Ku baiwa marayu dukiyoyinsu (idan sun balaga,) kadaku ,musanya haramun da halal (kadaku ,karɓi mai kyau daga dukiyar maraYaku bashi mummuna,) kada kuci dukiyoyinsu (abar tarawa) izuwa dukiyoyinku, haƙiƙa shi (cin dukiyarsu) ya kasance zunubi ne maigirma.

(KIDIDDIGAR MATAYE DA ADALCI TAREDASU)

3. In kunji tsoron cewa bazaku iya adalci a cikin marayu ba, (kuma kukaji tsoron bazaku iya adalci a tsakanin matayenku ba,) to, ku auri daga abinda ya daɗaɗa na daga mataye, biyu-biyu, ko uku-uku ko hudu-hudu (hadaku, ƙara a kan haka). To, in kunji tsoron bazakuyi adalci (tsakaninsu a wajen ciyarwa da rabon kwana ba , to, ku auri guda ɗaya, koku takaita a kan abinda hannunku ya mallaka (na daga kuyangi,) wancananka shi yafi kusa da bakwayi zalunci ba.
4. Kuba mata sadakinsu kyautada daɗin rai, idan ranku ta daɗaɗa da wani abu nasa, to, kuci shi mai daɗi mai garɗi a makogwaro

(LOKACIN DA ZAMU BA MARAYU DUKIYARSU)

5. Kadaku ,baiwa wawaye (dukiyoyinsu) dasuke hannunku, wacce Allah yasanya ta rayuwa a gareku, ku azurta su daga cikinta, ku tufatar dasu, ku gaya musu magana abar sani (kuce):"Zamu baku dukiyarku idan kunyi hankali)".
6. Ku jarraba marayu har idan sun balaga (da mafarki ko da shekaru sha takwas gun maliki. sha biyar gun shafi'i) to, idan kun ga alamar shiriya daga garesu, to, ku bada dukiyoyinsu a garesu, kadaku ,cinye ta (yaku waɗannan waliyyai) don al-mubazzaranci, kuce muyi maza -maza kadasu girma. Wanda ya kasance mawadaci. daga cikinku, to, ya kame kansa (ga barin cin dukiyar maraya) wanda ya kasance mabuƙaci to, yaci da abin sani (gwargwadon Ladan aikinsa,) to, idan kun miƙa dukiyoyinsu izuwa garesu, to, ku shaidar a kansu, Allah ya isa mai kiyayewa da aikin halitta.

(TABBATAR DA GADO GA MAZAJE DA MATAYE)

لِّلرِّجَالِ نَصِيبٌ مِّمَّا تَرَكَ ٱلْوَٰلِدَٰنِ وَٱلْأَقْرَبُونَ وَلِلنِّسَآءِ
نَصِيبٌ مِّمَّا تَرَكَ ٱلْوَٰلِدَٰنِ وَٱلْأَقْرَبُونَ مِمَّا قَلَّ مِنْهُ أَوْ كَثُرَ
نَصِيبًا مَّفْرُوضًا ﴿7﴾ وَإِذَا حَضَرَ ٱلْقِسْمَةَ أُوْلُواْ ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَٰمَىٰ
وَٱلْمَسَٰكِينُ فَٱرْزُقُوهُم مِّنْهُ وَقُولُواْ لَهُمْ قَوْلًا مَّعْرُوفًا ﴿8﴾
وَلْيَخْشَ ٱلَّذِينَ لَوْ تَرَكُواْ مِنْ خَلْفِهِمْ ذُرِّيَّةً ضِعَٰفًا
خَافُواْ عَلَيْهِمْ فَلْيَتَّقُواْ ٱللَّهَ وَلْيَقُولُواْ قَوْلًا سَدِيدًا ﴿9﴾ إِنَّ
ٱلَّذِينَ يَأْكُلُونَ أَمْوَٰلَ ٱلْيَتَٰمَىٰ ظُلْمًا إِنَّمَا يَأْكُلُونَ فِي بُطُونِهِمْ نَارًا
وَسَيَصْلَوْنَ سَعِيرًا ﴿10﴾ * يُوصِيكُمُ ٱللَّهُ فِي أَوْلَٰدِكُمْ ثمن
لِلذَّكَرِ مِثْلُ حَظِّ ٱلْأُنثَيَيْنِ فَإِن كُنَّ نِسَآءً فَوْقَ ٱثْنَتَيْنِ فَلَهُنَّ
ثُلُثَا مَا تَرَكَ وَإِن كَانَتْ وَٰحِدَةً فَلَهَا ٱلنِّصْفُ وَلِأَبَوَيْهِ لِكُلِّ
وَٰحِدٍ مِّنْهُمَا ٱلسُّدُسُ مِمَّا تَرَكَ إِن كَانَ لَهُۥ وَلَدٌ فَإِن لَّمْ
يَكُن لَّهُۥ وَلَدٌ وَوَرِثَهُۥ أَبَوَاهُ فَلِأُمِّهِ ٱلثُّلُثُ فَإِن كَانَ لَهُۥ
إِخْوَةٌ فَلِأُمِّهِ ٱلسُّدُسُ مِنۢ بَعْدِ وَصِيَّةٍ يُوصِي بِهَا أَوْ دَيْنٍ
ءَابَآؤُكُمْ وَأَبْنَآؤُكُمْ لَا تَدْرُونَ أَيُّهُمْ أَقْرَبُ لَكُمْ
نَفْعًا فَرِيضَةً مِّنَ ٱللَّهِ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا حَكِيمًا ﴿11﴾

7. Maza suna da rabo daga abinda mahaifa da makusanta suka bari, mata ma suna da rabo (daga abinda iyaye suka bari da makusanta) daga abinda ya ƙaranta daga gareshi koya yawaita, rabo abin wajabtawar (miƙa shi izuwa garesu).

(BĀDA WANI ABU GA "YAN'UWA BA MASU GADO BA GABAN RABO)

8. Idan "yan 'uwa da marayu da miskinai suka halarci wurin rabon gado, to. ku basu wani abu daga gareshi. ku faɗa musu magana Mai kyau. (kuce: "Ba namu bane na yara ne" yin haka mandubi ne ba wajibi ba, bakuma mansuhi ba, duba Sawi

(YADDA KAYI HAKA ZA AYI MAKA)

9. Waɗanda in sun bar zuriya raunana a bayansu suke Jin tsoron tozartarsu suji tsoron Allah (a kan marayu) suji tsoron Allah dai (a cikin al'amarin marayu, suyi masu abinda suke so ayiwa zuriyarsu bayansu,) su faɗi magana madaidaiciya (ga majiyyaci du marayu, su umarce shi yayi sadaka da koma bayan sulusi, suce da marayu:"Kadaku ,damu, mu kamar iyayenku muke)".

(WA'AZI A KAN CIN DUKIYAR MARAYU)

10. Haƙiƙa waɗanda suke cin dukiyar marayu don zalunci. suna cin wuta bal-bal ne a cikin cukkunansu kawai, da sannu zasu shiga wuta mai tsananin zafi

11. Allah yana umarninku a cikin (sha'anin)"ya" yayanku (da abindaza a ambata); .Namiji yana da misalin rabon mace biyu (in sun haɗu dashi. shida rabi su biyu da rabi). Idan ko mataye ne kawai, fiye da biyu, to, suna dasulusanin abinda matacce ya bari, (wato kashi biyu daga uku). Idan ya zama ita ɗayace to, rabi na gare ta. Ga iyayensu kuma kowane ɗaya daga garesu yana dasudusi (ɗaya daga shida) da matacce ya bari, in yana da (ɗa namiji, to, idan kuwa bashida ɗa, iyayensa suka gaje shi kawai, to, sulusi yana ga uwarsa (wato ɗaya daga uku). Idan yana da "yan"uwa mazaje (daga biyu zuwa abinda yayi sama,) to, sudusi naga uwarsa, (wato ɗaya daga shida) bayan zartar da wasiyya dayayi ko kuma biyan bashi, amma da bashi za a fara). Iyayenkuda "ya"yayenku baku sani ba wannenansu mafi kusancin amfani a gareku, a duniya da lahira,(da yawa mai zaton ɗansa yafi amfani gareshiya bashi gado, ubaya zama'mafi amfani, haka nan kuma sunkuye, Allah ne yasan mafi amfani, saboda haka yajiɓinci raba gado da kansa,) rabo abin yankowa daga Allah, haƙiƙa Ubanglji masanine (da halitta) gwanine (cikin abinda ya shirya musu).

وَلَكُمْ نِصْفُ مَا تَرَكَ أَزْوَاجُكُمْ إِن لَّمْ يَكُن لَّهُنَّ وَلَدٌ
فَإِن كَانَ لَهُنَّ وَلَدٌ فَلَكُمُ الرُّبُعُ مِمَّا تَرَكْنَ مِنۢ بَعْدِ
وَصِيَّةٍ يُوصِينَ بِهَا أَوْ دَيْنٍ وَلَهُنَّ الرُّبُعُ مِمَّا تَرَكْتُمْ
إِن لَّمْ يَكُن لَّكُمْ وَلَدٌ فَإِن كَانَ لَكُمْ وَلَدٌ فَلَهُنَّ
الثُّمُنُ مِمَّا تَرَكْتُم مِّنۢ بَعْدِ وَصِيَّةٍ تُوصُونَ بِهَا أَوْ دَيْنٍ
وَإِن كَانَ رَجُلٌ يُورَثُ كَلَالَةً أَوِ امْرَأَةٌ وَلَهُ
أَخٌ أَوْ أُخْتٌ فَلِكُلِّ وَاحِدٍ مِّنْهُمَا السُّدُسُ
فَإِن كَانُوا أَكْثَرَ مِن ذَٰلِكَ فَهُمْ شُرَكَاءُ
فِي الثُّلُثِ مِنۢ بَعْدِ وَصِيَّةٍ يُوصِي بِهَا أَوْ دَيْنٍ
غَيْرَ مُضَارٍّ وَصِيَّةً مِّنَ اللَّهِ وَاللَّهُ عَلِيمٌ حَلِيمٌ ﴿12﴾
ربع * تِلْكَ حُدُودُ اللَّهِ وَمَن يُطِعِ اللَّهَ وَرَسُولَهُ نُدْخِلْهُ
جَنَّاتٍ تَجْرِي مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَارُ
خَالِدِينَ فِيهَا وَذَٰلِكَ الْفَوْزُ الْعَظِيمُ ﴿13﴾
وَمَن يَعْصِ اللَّهَ وَرَسُولَهُ وَيَتَعَدَّ حُدُودَهُ
نُدْخِلْهُ نَارًا خَالِدًا فِيهَا وَلَهُ عَذَابٌ مُّهِينٌ ﴿14﴾

12. Rabin abinda matanku suka bari yana gareku in basuda ɗa. (naku ko na waninku). Idan suna da ɗa, to, rubu'i na gareku (wato ɗaya daga hudu,) daga abinda suka bari, bayan wasiyya da sukayi wasiyya da ita, ko bashi. Rubu'in na garesu daga abinda kuka bari in bakuda ɗa daga garesu ko daga waninsu, in ko kuna da ɗa to, sumuni yana ga matayen nan, (wato daya daga cikin takwas) daga abinda kuka bari, bayan wasiyya da sukayi wasiyya da ita ko bashi. Idan ya zama mutumne daza a gaje shi bakarara, (ba uba baɗa) ko mace (bakarara) alhali yana da ɗan'uwa namiji ko "yar'uwa ta mace, to, sudusi ya tabbata ga kowane ɗaya daga garesu, (daga abinda ya bari). To, in sun kasance mafi yawa daga haka, to, su masu tarayya ne a cikin sulusi, (namiji da mace duk ɗaya ne a ciki,) bayan wasiyar dayayi wasiyya da ita ko bashi, ba abin shigarwa da cuta ba, (wato ba mai shigar da cuta a kan magada ba, shine yayi wasiyya da mafi yawa daga sulusi). Wasiyyace daga Allah, Allah masanine (da halitta) mai jinkirin azabane (ga wanda ya saɓe shi).

(SAKAMAKON WANDA YA KIYAYE HADDODIN ALLAH DA MA'AIKINSA DA NARKO GA WANDA YA SABE SU

13. Waɗancananka iyakokin Allah ne, (wato waɗancan hukunce-hukuncen, na al'amarin marayu da abinda yake bayansa, iyakokin Allah ne daya iyakance ga bayinsa, donsuyi aiki dasu kadasu ƙetare). Wanda yabi Allah da manzonsa (cikin abinda yayi hukunci dashi) zai shigar dashi aljannatai waɗanda ƙoramu suke kwarara daga ƙarƙashinsu, masu dauwama a cikinsu. Wancananka shine rabo maigirma.
14. Wanda ya saɓi Allah da manzonsa, ya ƙetare iyakokinsa, ma shigar dashi wuta mai dauwama a cikinta. azaba mai wula -ƙantarwa na gareshi.

(FASIƘANCI DA SAKAMAKONSA)

وَالَّٰتِي يَأْتِينَ الْفَاحِشَةَ مِن نِّسَآئِكُمْ فَاسْتَشْهِدُواْ عَلَيْهِنَّ
أَرْبَعَةً مِّنكُمْ فَإِن شَهِدُواْ فَأَمْسِكُوهُنَّ فِي الْبُيُوتِ
حَتَّىٰ يَتَوَفَّىٰهُنَّ الْمَوْتُ أَوْ يَجْعَلَ اللَّهُ لَهُنَّ سَبِيلاً (15) وَالَّذَانِ
يَأْتِيَٰنِهَا مِنكُمْ فَـَٔاذُوهُمَا فَإِن تَابَا وَأَصْلَحَا
فَأَعْرِضُواْ عَنْهُمَا إِنَّ اللَّهَ كَانَ تَوَّاباً رَّحِيماً (16)
إِنَّمَا التَّوْبَةُ عَلَى اللَّهِ لِلَّذِينَ يَعْمَلُونَ السُّوٓءَ
بِجَهَالَةٍ ثُمَّ يَتُوبُونَ مِن قَرِيبٍ فَأُوْلَٰٓئِكَ يَتُوبُ اللَّهُ
عَلَيْهِمْ وَكَانَ اللَّهُ عَلِيماً حَكِيماً (17) وَلَيْسَتِ
التَّوْبَةُ لِلَّذِينَ يَعْمَلُونَ السَّيِّـَٔاتِ حَتَّىٰ إِذَا حَضَرَ أَحَدَهُمُ
الْمَوْتُ قَالَ إِنِّي تُبْتُ ءَالَٰنَ وَلَا الَّذِينَ يَمُوتُونَ وَهُمْ كُفَّارٌ
أُوْلَٰٓئِكَ أَعْتَدْنَا لَهُمْ عَذَاباً أَلِيماً (18) * يَٰٓأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُواْ
لَا يَحِلُّ لَكُمْ أَن تَرِثُواْ النِّسَآءَ كَرْهاً وَلَا تَعْضُلُوهُنَّ
لِتَذْهَبُواْ بِبَعْضِ مَآ ءَاتَيْتُمُوهُنَّ إِلَّا أَن يَأْتِينَ بِفَاحِشَةٍ
مُّبَيِّنَةٍ وَعَاشِرُوهُنَّ بِالْمَعْرُوفِ فَإِن كَرِهْتُمُوهُنَّ فَعَسَىٰ
أَن تَكْرَهُواْ شَيْـًٔا وَيَجْعَلَ اللَّهُ فِيهِ خَيْراً كَثِيراً (19)

ثمن

15. Wađannan dasuke aikata zina daga cikin matayanku, to, ku shaidar da shaidu hudu a kansu. daga cikinku (mazamusulmi) to, idan suka shaida (a kansu da ita) to, ku tsare su a cikin đakuna (wato, ku hana su cuđanya da mutane,) har mutuwa tazo masu, ko kuma Ubangiji yasanya tafarkin (fita) a garesu, (an umarce su da wannan a farkon Musulunci ne sannan aka sa suyiwa budurwa bulala đari da nisanta ta daga gari, da kuma jefe katangattacciya).

16. Wađannan kuma dasuke aikata ta (wato zina ko Luwađi) daga cikinku, (mazaje,) to, ku cuce su (da zagi da duka da takalma,) to in suka tubasukayi kyakkyawan aiki. to, ku rabu dasu, Haƙiƙa Ubangiji ya kasance mai yawan karɓar tuba (ga wanda ya tuba,) mai jinkai (dashi wannan hukunci, shafaffe ne da haddi, wato, rajamu).

(YAUSHE ALLAH YAKE KARBAR TUBA?)

17. Dahir karɓar tubaya tabbata ga wađanda suke aikata saɓo batareda sani ba, sannan su tubadaga kusa, (tun gaban gargara wato ƙarshen numfashi, ai rai batazo maƙogwaro ba,) Ubangiji ya tabbata masani da hallittarsa gwani cikin aikinsa.

18. Tuba bata kasance ga wađannan dasuke aikata zunubai ba, har yayin da mutuwa ta zowa đayansu, sai yace "haƙiƙa ni na tuba a yanzi(,"(to, wannan tuba bazata amfane shiba,) wala wađannan dasuke mutuwa suna kafirai, (idan sun tuba a Lahira. yayin ganin azaba) wađancananka mun tanadi azaba mai rađađi a garesu.

(ƘAƘA ZAMUYI MU'AMALA DA MATAMMU)

19. Yaku wađanda kuka bada gaskiya! bai halatta gareku ku gaji mata tilas ba, (sun kasance a jahiliyya suna gadon matan "yan'uwansu in sun ga dama su auresu ba tareda sadaki ba. ko su aurar dasu su karɓi sadakinsu ko su hana su auri wađanđa suke so sai sun basu kuđi. ko su mutu su gaje su). Kadaku ,hanasu su auri waninku, (wato ku tsaresu a wurinku donku cucesu) don kutafi da ba'alin abinda kuka basu (daga sadaki,) sai in sun aikata ɓarna mabayyaniya, kuyi mu'amala dasu da kykkyawar (magana da ciyarwa da makwanci masu kyau). To. in kunƙi su, to. (ku daure,) yana kusanta kuƙi abu Allah yasanya alheri mai yawa a cikinsa, (da nagari ko waninsa).

وَإِنْ أَرَدتُّمُ اُ۪سْتِبْدَالَ زَوْجٍ مَّكَانَ زَوْجٍ وَءَاتَيْتُمُۥ
إِحْدَىٰهُنَّ قِنطَاراً فَلَا تَأْخُذُواْ مِنْهُ شَيْـًٔاۖ أَتَأْخُذُونَهُۥ
بُهْتَاناً وَإِثْماً مُّبِيناًۖ ﴿20﴾ وَكَيْفَ تَأْخُذُونَهُۥ وَقَدْ أَفْضَىٰ
بَعْضُكُمُۥ إِلَىٰ بَعْضٍ وَأَخَذْنَ مِنكُم مِّيثَاقاً غَلِيظاًۖ ﴿21﴾
وَلَا تَنكِحُواْ مَا نَكَحَ ءَابَآؤُكُم مِّنَ اَ۬لنِّسَآءِ
إِلَّا مَا قَدْ سَلَفَۖ إِنَّهُۥ كَانَ فَٰحِشَةً وَمَقْتاً وَسَآءَ
سَبِيلاًۖ ﴿22﴾ حُرِّمَتْ عَلَيْكُمُۥ أُمَّهَٰتُكُمُۥ وَبَنَاتُكُمُۥ وَأَخَوَٰتُكُمُۥ
وَعَمَّٰتُكُمْ وَخَٰلَٰتُكُمْ وَبَنَاتُ اُ۬لْأَخِ وَبَنَاتُ اُ۬لْأُخْتِۖ
وَأُمَّهَٰتُكُمُ اُ۬لَّٰتِےٓ أَرْضَعْنَكُمُۥ وَأَخَوَٰتُكُم مِّنَ
اَ۬لرَّضَٰعَةِۖ وَأُمَّهَٰتُ نِسَآئِكُمْ وَرَبَٰٓئِبُكُمُ
اُ۬لَّٰتِے فِے حُجُورِكُم مِّن نِّسَآئِكُمُ اُ۬لَّٰتِے دَخَلْتُم
بِهِنَّۖ فَإِن لَّمْ تَكُونُواْ دَخَلْتُم بِهِنَّ
فَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمُۥۖ وَحَلَٰٓئِلُ أَبْنَآئِكُمُ اُ۬لَّذِينَ
مِنْ أَصْلَٰبِكُمْۖ وَأَن تَجْمَعُواْ بَيْنَ اَ۬لْأُخْتَيْنِ
إِلَّا مَا قَدْ سَلَفَۖ إِنَّ اَ۬للَّهَ كَانَ غَفُوراً رَّحِيماًۖ ﴿23﴾

20. In kun nufi musaya mace maimakon wata mace, (shine kuka saketa,) alhali kun baiwa ɗayarsu dukiya mai tsoka, to. kadaku ,ƙarbi wani abu daga gareshi. Donme zaku karɓe shi don zalunci da zunubi mabayyani?.
21. Ta yaya zaku karɓo shi. alhali ba'alinku ya sadu da ba'ali (da tarawa wanda yake tabbatar da sadaki.) kuma sun riƙi alƙawari mai (ƙarfi daga gareku, (shine abinda Allah yayi umarni dashi na daga riƙe su da abin sani ko sakin su da kyautatawa).

(WAƊANDA AURENSU YA HARAMANTA)

22. Kadaku ,auri waɗanda iyayenku suka aura na daga mata, sai abinda ya wuce (zamanin jahiliyya, anyi muku afuwarsa, zamanin jahiliyya sun kasance suna auren abinda iyayensu suka bari na daga mataye). Haƙiƙa wannan aure ya kasance mummuna da sababin kyara daga Allah. ya munana tafarki.
23. An haramta muku iyayenku matada "ya"yanku mataye, da "yan"uwanku mataye, (najihar uwa ko uba.) da "yan'uwan babanninku. mataye. da kuma "yan'uwan uwayenku mataye da "ya"yan ɗan uwa mataye da" ya"yan "yar'uwa ta mace. da iyayenku waɗanda suka shayar daku nono da "yan"uwanku mata na shan nono, da iyayen matankuda "ya"yayen matarku, (wato agola,) waɗanda suke cikin rainon ku na daga matayenku waɗanda kuka tara dasu, in baku kasance kun tara dasu ba, to, ba Laifi a gareku (a cikin auren "ya"yensu, in kun rabu da iyayen) da matayen "ya"yanku waɗanda suke daga tsatsonku kuma (an haramta muku) ku tara tsakanin "yan"uwa guda biyu)na nasabako na shan nono,) sai abinda ya wuce (aja-hiliyya). Haƙiƙa Ubangiji ya kasance mai gafara ne (ga abinda ya wuce gaban hani,) mai jinƙai daku (a cikin wannan).

(WANI ABU NA DAGA HUKUNCE-HUKUNCEN AURE)

حزب

۞ وَالْمُحْصَنَٰتُ مِنَ النِّسَآءِ إِلَّا مَا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُكُمْ
كِتَٰبَ اللَّهِ عَلَيْكُمْ وَأُحِلَّ لَكُم مَّا وَرَآءَ ذَٰلِكُمْ
أَن تَبْتَغُوا بِأَمْوَٰلِكُم مُّحْصِنِينَ غَيْرَ مُسَٰفِحِينَ فَمَا اسْتَمْتَعْتُم
بِهِۦ مِنْهُنَّ فَـَٔاتُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ فَرِيضَةً وَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ
فِيمَا تَرَٰضَيْتُم بِهِۦ مِنۢ بَعْدِ الْفَرِيضَةِ إِنَّ اللَّهَ كَانَ عَلِيمًا
حَكِيمًا ﴿24﴾ وَمَن لَّمْ يَسْتَطِعْ مِنكُمْ طَوْلًا أَن يَنكِحَ الْمُحْصَنَٰتِ
الْمُؤْمِنَٰتِ فَمِن مَّا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُكُم مِّن فَتَيَٰتِكُمُ
الْمُؤْمِنَٰتِ وَاللَّهُ أَعْلَمُ بِإِيمَٰنِكُم بَعْضُكُم مِّنۢ بَعْضٍ
فَانكِحُوهُنَّ بِإِذْنِ أَهْلِهِنَّ وَءَاتُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ
بِالْمَعْرُوفِ مُحْصَنَٰتٍ غَيْرَ مُسَٰفِحَٰتٍ وَلَا مُتَّخِذَٰتِ
أَخْدَانٍ فَإِذَا أُحْصِنَّ فَإِنْ أَتَيْنَ بِفَٰحِشَةٍ فَعَلَيْهِنَّ نِصْفُ
مَا عَلَى الْمُحْصَنَٰتِ مِنَ الْعَذَابِ ذَٰلِكَ لِمَنْ خَشِيَ الْعَنَتَ
مِنكُمْ وَأَن تَصْبِرُوا خَيْرٌ لَّكُمْ وَاللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿25﴾
يُرِيدُ اللَّهُ لِيُبَيِّنَ لَكُمْ وَيَهْدِيَكُمْ سُنَنَ الَّذِينَ
مِن قَبْلِكُمْ وَيَتُوبَ عَلَيْكُمْ وَاللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿26﴾

24. Ubangjij ya haramta muku katangantattu (wato) masu mazaje daga mataye (kadaku ,aure su sai sun rabu da mazajensu,) sai abinda hannunku ya mallaka (na kuyangi, wadanda aka ribato su a yaki, halaccinsu yana nasuwa, izuwa zuriyarsu, muddan ba a "yantasu "yantuwa ta sha-ri'a ba, "yancin dole ba "yancin shari'a ba ne) Allah ya rubuta wannan rubutuwa a kanku. Ya halarta muku wanin wancananku (shine ku nemi matam da dukiyoyinkuda sadaki ko da mallaka) kuma masu aure ba masu zina ba, to, wadanda kukaji dadi dasu daga cikinsu. (da taki ko madakinsa) to, ku basu sadakinsu, wanda kuka kaddara musu abin wajabtawa. babu Laifi a gareku a abinda kukayi yarjejeniya dashi bayan abin yankawar nan (na saryarwa ko ragewa ko karawa) hakika Ubangiji ya tabbata masani (da halitta) gwani (cikin abinda ya shirya).

(YAUSHE NE AKE AUREN KUYANGA, MENENE SAKAMAKONTA IN TAYI ZINA

25. Wanda bai sami ikon ya auri "ya" ya katangantattu muminai ba, to saiya aura daga abinda hannunku ta mallaka na daga kuyanginku muminai, Allah ne masani da imaninku, (ku isa da zahirinsa, kubarwa Allah sanin asirin boye, da yawa kuyangar da tafi "ya,) ba'alinku daga ba'ali yake (daidai kuke a cikin addini, kada kuyi kyamar auren kuyangi,) to, ku aure su da izinin waliyyansu, ku basu sadakansu, da a bin sani (ga shari'a bada taurin bashi ba. bada ragewa ba) suna kamammu ba masu zina a fili ba, ba masu rikon abokai masu zina dasu ba a, boye wato kwartaye yi aure) to in suka aikata zina to. idan an katangance su. (wato kwartaye) to idan an katangance su (wato sukayi aure) tu. in suka aikata zina to, rabin abinda yake kan 'ya'ya katangantattu na garesu na daga haddi, (sai ai musu bulala hamsin a nisanta su shekara), wannan (hukunci na halaccin auren kuyangi) ga wanda yaji tsoron zina daga gareku. Amma ku daure (ga barin aurensu) shi yafi amfani gareku. don kada danku ya zama bawa). Allah mai gafara ne mai jinkai (ya yalwata muku a cikin wanna).

(HIKIMOMI NA HUKUNCE-HUKUNCEN DA SUKA WUCE DA BAKAR ANIYAR TURAWA GAMI DAMU)

26. Ubangiji yana nufin ya bayyana muku (shari'o'in addninkune da matsalolin al'amuranku) ya shirye ku hanyoyin wadanda suke gabanku (na daga Annabawa; a cikin halacci da haramci don ku kwaikwaye su,) kuma ya karbi tuban ku, Allah masanine (daku,) gwanine (cikin abinda ya shirya).

وَاللَّهُ يُرِيدُ أَن يَتُوبَ عَلَيْكُمْ وَيُرِيدُ الَّذِينَ
يَتَّبِعُونَ الشَّهَوَاتِ أَن تَمِيلُوا مَيْلًا عَظِيمًا 27 يُرِيدُ
اللَّهُ أَن يُخَفِّفَ عَنكُمْ وَخُلِقَ الْإِنسَانُ ضَعِيفًا 28
يَا أَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُوا لَا تَأْكُلُوا أَمْوَالَكُم بَيْنَكُم
بِالْبَاطِلِ إِلَّا أَن تَكُونَ تِجَارَةٌ عَن تَرَاضٍ مِّنكُمْ
وَلَا تَقْتُلُوا أَنفُسَكُمْ إِنَّ اللَّهَ كَانَ بِكُمْ رَحِيمًا 29 وَمَن
يَفْعَلْ ذَٰلِكَ عُدْوَانًا وَظُلْمًا فَسَوْفَ نُصْلِيهِ نَارًا وَكَانَ ذَٰلِكَ
عَلَى اللَّهِ يَسِيرًا 30 * إِن تَجْتَنِبُوا كَبَآئِرَ مَا تُنْهَوْنَ عَنْهُ نُكَفِّرْ
عَنكُمْ سَيِّئَاتِكُمْ وَنُدْخِلْكُم مَّدْخَلًا كَرِيمًا 31
وَلَا تَتَمَنَّوْا مَا فَضَّلَ اللَّهُ بِهِ بَعْضَكُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ
لِّلرِّجَالِ نَصِيبٌ مِّمَّا اكْتَسَبُوا وَلِلنِّسَآءِ نَصِيبٌ مِّمَّا اكْتَسَبْنَ
وَسْئَلُوا اللَّهَ مِن فَضْلِهِ إِنَّ اللَّهَ كَانَ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمًا 32
وَلِكُلٍّ جَعَلْنَا مَوَالِيَ مِمَّا تَرَكَ الْوَالِدَانِ
وَالْأَقْرَبُونَ وَالَّذِينَ عَقَدَتْ أَيْمَانُكُمْ فَـَٔاتُوهُمْ
نَصِيبَهُمْ إِنَّ اللَّهَ كَانَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ شَهِيدًا 33

ثمن

27. Ubangiji yana nufi ya karɓi tubanku, amma waɗanda suke bin sha'awace-sha'awace, (Yahudu da Nasara da sauransu) suna so ku karkata karkata maigirma (ga barin gaskiya sabodaku ,zama kamar su. A nanfa Ubangiji yayi mana tambihi gameda halinda muke ciki a yanzu tareda daulolin Yamma, suna son mu saki Allah donya sake mu, Allah ya sawwake, amin).
28. Allah yana nufi ya sawwake muku (hukunce-hukuncen shari'a,) an halicci mutum rarrauna (bazai iya haƙuri ga barin matada sha'awa ba, da kaidin waɗannan kafirai ba).

(HARAMCIN CIN DUKIYA TA MUMMNAR HANYA DA JEFA KAI CIKIN GARARI)

29. ya waɗanda suka bada gaskiya' kada kuci dukiyoyinku tsakaninku ta mummunar hanya. saiko ta zama ciniki dayarjejeniya daga garekuda daɗin rai. kadaku ,kashe kanku. Ubangiji ya tabbata mai jinƙai (daku).
30. Wanda ya aikata (wani abu daga) wannan. don shisshigi da zalunci, da sannu zamu shigar dashi wuta, wancananka ya kasance mai sauƙi bisa ga Allah.

(SAKAMAKON BARIN SABO)

31. In kun nisanci manya–manyan abinda aka hanaku ga barinsa. (kamar kisan kai da zina da sata, (Ibni Abas yace adadin kaba'ira Yakusa da saba'in) ma kankare miyagun ayyukanku (na saga'irai) ga barin ku, ma shigar daku ma shiga maigirma Aljanna.

(HANI GA BARIN HASSADA DA KWADAITARWA AKAN AIKI TUƘURU)

32. Kadaku ,guraci gushewar abinda Allah yafifita ba'alinku dashi a kan ba'ali, maza sunada sakamaku na daga abinda suka aikata (na jihadi) mata suna da rabo (na daga abinda suka aikata, na bin mazajensu da kiyaye farjojinsu da waninsa) Allah ya faɗi haka ne yayin da Ummu Salmata tace. ina ma mazaje ne mu muyi jihadi, mu sami ladar irin na maza!) Ku roƙi Allah daga falalarsa (abinda kuke buƙata sai yabaku) Haƙiƙa Ubangiji ya tabbata masani da kome.

(BAIWA KOWANE MAI HAƘƘI HAƘƘINSA)

33. Mun sanya magada ga kowan (ɗaya daga mazaje da mataye) daza a ba su daga abinda iyaye suka bari da makusanta waɗanda hannuwan ku ta ƙudura rantsuwa da su (a jahiliyya a kan taimako da gabo)to ku basu rabonsu (a yanzu na daga gado sudusi) hƙiƙa Ubangiji ya tabbata mai tsinkaye ne bisa kome (wannan shafaffe ne da faɗin Ubangiji WA'ULUL ARHAMI)

(FIFITA MAZA KAN MATA)

ٱلرِّجَالُ قَوَّٰمُونَ عَلَى ٱلنِّسَآءِ بِمَا فَضَّلَ ٱللَّهُ
بَعْضَهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ وَبِمَآ أَنفَقُواْ مِنْ أَمْوَٰلِهِمْ
فَٱلصَّٰلِحَٰتُ قَٰنِتَٰتٌ حَٰفِظَٰتٌ لِّلْغَيْبِ بِمَا حَفِظَ ٱللَّهُ
وَٱلَّٰتِي تَخَافُونَ نُشُوزَهُنَّ فَعِظُوهُنَّ وَٱهْجُرُوهُنَّ
فِي ٱلْمَضَاجِعِ وَٱضْرِبُوهُنَّ فَإِنْ أَطَعْنَكُمْ
فَلَا تَبْغُواْ عَلَيْهِنَّ سَبِيلًا إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيًّا كَبِيرًا ﴿34﴾
وَإِنْ خِفْتُمْ شِقَاقَ بَيْنِهِمَا فَٱبْعَثُواْ حَكَمًا مِّنْ أَهْلِهِۦ
وَحَكَمًا مِّنْ أَهْلِهَآ إِن يُرِيدَآ إِصْلَٰحًا يُوَفِّقِ ٱللَّهُ بَيْنَهُمَآ
إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا خَبِيرًا ﴿35﴾ ۞ وَٱعْبُدُواْ ٱللَّهَ وَلَا تُشْرِكُواْ بِهِۦ
شَيْـًٔا وَبِٱلْوَٰلِدَيْنِ إِحْسَٰنًا وَبِذِي ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَٰمَىٰ
وَٱلْمَسَٰكِينِ وَٱلْجَارِ ذِي ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْجَارِ ٱلْجُنُبِ وَٱلصَّاحِبِ
بِٱلْجَنۢبِ وَٱبْنِ ٱلسَّبِيلِ وَمَا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُكُمْ إِنَّ ٱللَّهَ
لَا يُحِبُّ مَن كَانَ مُخْتَالًا فَخُورًا ﴿36﴾ ٱلَّذِينَ يَبْخَلُونَ
وَيَأْمُرُونَ ٱلنَّاسَ بِٱلْبُخْلِ وَيَكْتُمُونَ مَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ
مِن فَضْلِهِۦ وَأَعْتَدْنَا لِلْكَٰفِرِينَ عَذَابًا مُّهِينًا ﴿37﴾

ربع

34. Mazaje ababen salladawa ne a kan mata (su Ladabtar dasu, su duba harkokinsu,) saboda Allah yafifita maza a kansu da ilmi da walittaka da hankali da wanin wannan) kuma da abinda suka ciyar a kansu) na daga dukiyoyinsu.To managartan mata masu bine (ga mazajensu) masu kiyayewa ne a fakuwar (mijinsu da farjojinsu da waninsu,) saboda Allah ya kiyaye (su da yiwa maza wasiyya dasu) Wadanda kuke jin tsoron takadarancinsu, to, kuyi musu wa,azi, (ku tsoratar dasu azabar Allah,) ku kaurace musu a wuraren kwanciya (izuwa wata shimfida In sunci gabada takadaranci, to, in bai amfana ba) ku doke su duka ba mai cutarwa ba, idan suka biku a cikin abinda kuke nufi to, kadaku ,nemi hanya a kansu (ta sake dukan su ba gaira badalili'). Hakika Ubangiji ya tabbata madaukaki maigirma: kuji tsoransa kada yayi muku azaba in kun zalunce su.

(WANI TSARI NA TABBATAR DA ZAMAN LAFIYA)

35. In kun sami sabani tsakaninsu (su ma'aura) to, sai ku aiki mutum adali daga makusantan mijin, da mutum adali daga ahalinta, (miji ya wakkala nasa a cikin saki ko karbar wali, ita kuma ta wakkala nata a cikin hulu'u. su dubada kyau su gani) in sun nufi gyara, Allah zaiyi mawafaka tsakaninsu (su ma'auran). Ubangiji ya tabbata masani (da komai) masanin asirin take tamfar na sarari.

(WA'AZI DA IRSHADI)[1]

36. Ku bautawa Allah shi kadai. kadaku ,tara kome dashi. (ku kyautata) ga iyaye kyautatawa da ma'abocin zumunci da marayu da miskinai, da makwabci ma'abocin kusanci anasabako a makwabtak da makwabci ma'nisanci, a nasabako a mak-wabtaka da aboki a dab dakai (a tafiyako a sana'a, ko matarka) da dan tafarki (wanda guzuri ya sare masa) da abinda hannayenku suka mallaka. Hakika Ubangiji bayason wanda ya kasance mai girman kai mai fariya (ga mutane da abinda aka bashi na ni'ima).

37. Wadanda suke rowa (da abinda ya wajaba a kansu,) suke umarnin mutane da rowa (dashi) suke boye abinda Allah ya basu, na daga falalarsa, (na ilimi da dukiya, narko mai tsanani yana garesu (sune Yahudu da makamantansu) Mun tanadi azaba mai wulakantarwa ga kafirai.

(1) Shiryarwa.

وَالَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمْوَالَهُمْ رِئَاءَ النَّاسِ وَلَا يُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ
وَلَا بِالْيَوْمِ الْآخِرِ وَمَن يَكُنِ الشَّيْطَانُ لَهُ قَرِينًا فَسَاءَ قَرِينًا ﴿38﴾
وَمَاذَا عَلَيْهِمْ لَوْ آمَنُوا بِاللَّهِ وَالْيَوْمِ الْآخِرِ وَأَنفَقُوا مِمَّا
رَزَقَهُمُ اللَّهُ وَكَانَ اللَّهُ بِهِمْ عَلِيمًا ﴿39﴾ إِنَّ اللَّهَ لَا يَظْلِمُ
مِثْقَالَ ذَرَّةٍ وَإِن تَكُ حَسَنَةً يُضَاعِفْهَا وَيُؤْتِ مِن
لَّدُنْهُ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿40﴾ فَكَيْفَ إِذَا جِئْنَا مِن كُلِّ
أُمَّةٍ بِشَهِيدٍ وَجِئْنَا بِكَ عَلَىٰ هَٰؤُلَاءِ شَهِيدًا ﴿41﴾ يَوْمَئِذٍ
يَوَدُّ الَّذِينَ كَفَرُوا وَعَصَوُا الرَّسُولَ لَوْ تُسَوَّىٰ بِهِمُ الْأَرْضُ
وَلَا يَكْتُمُونَ اللَّهَ حَدِيثًا ﴿42﴾ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا لَا تَقْرَبُوا
الصَّلَاةَ وَأَنتُمْ سُكَارَىٰ حَتَّىٰ تَعْلَمُوا مَا تَقُولُونَ وَلَا جُنُبًا
إِلَّا عَابِرِي سَبِيلٍ حَتَّىٰ تَغْتَسِلُوا وَإِن كُنتُم مَّرْضَىٰ أَوْ عَلَىٰ سَفَرٍ
أَوْ جَاءَ أَحَدٌ مِّنكُم مِّنَ الْغَائِطِ أَوْ لَامَسْتُمُ النِّسَاءَ فَلَمْ تَجِدُوا
مَاءً فَتَيَمَّمُوا صَعِيدًا طَيِّبًا فَامْسَحُوا بِوُجُوهِكُمْ وَأَيْدِيكُمْ إِنَّ اللَّهَ
كَانَ عَفُوًّا غَفُورًا ﴿43﴾ أَلَمْ تَرَ إِلَى الَّذِينَ أُوتُوا نَصِيبًا مِّنَ الْكِتَابِ
يَشْتَرُونَ الضَّلَالَةَ وَيُرِيدُونَ أَن تَضِلُّوا السَّبِيلَ

38. Da wad̄anda suke ciyar da dukiyoyinsu don riyaga mutane basa bada gaskiya da Allah da ranar Lahira (suma narko mai tsanani ya tabbata garesu).Wanda Shaid̄an ya kasance abokinsa, (yake bin umarnin Shaid̄an) to, tir da aboki!
39. Menene Laifi garesu dasun bada gaskiya da Allah da ranar Lahira suka ciyar daga abinda Allah ya azurta musu? Ubangiji dai masanine dasu.

(TSORATARWA DA KWADAITARWA)

40. Haƙiƙa Ubangiji baya zaluntar (kowa) misalin ƙwayar komayya, in hasana ta tabbata saiya ninka ta (daga goma izuwa d̄ari bakwai) yabada Lada maigirma (daga gareshi wanda ba wanda yasan gwargwadonsa, sai Allah).
41. To, ƙaƙa zasuyi, idan muka zoda mai shaida daga kowace al'umma (dazai shaida a kantada aikinta shine Annabinta) muka zodakai (Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama) shaida a kan wad̄annan?
42. Ranar nan wad̄anda suka kafirta suka saɓi manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) zasuyi gurin dama an daidaita ƙasa dasu. (su zama turbaya, saboda girman tsoro,) kuma (suyi gurin da) basu ɓoyewa Allah zance ba!

(BA'ALIN SHARUDDAN SALLAH TAREDA BAYANIN RAHUSAR [1] TAIMANA)

43. yaku wad̄anda suka bada gaskiya! kadaku ,kusanci sallah alhali kuna masu maye, sai kun san abinda kuke fad̄a (kun wartsake. Kadaku ,kusance ta) kuna masu janaba, sai koku masu ketare tafarki ne matafiya, sai kunyi wanka, (watau kadaku ,zauna a cikin masallaci, sai dai ko wucewa ba tareda zama ba) in kun kasance marasa Lafiya, (rashin Lafiyar da ruwa zai cuce ta) ko kuna kan tafiya (alhali kuna da janaba, ko kari ƙarami) ko d̄ayanku yazo daga ban d̄aki. ko kuka tara da mata, baku samu ruwa ba (wanda zakuyi wanka dashi bayan bincikawa) to, ku nufi turɓaya tsatstsarka (ku taɓa ta sau biyu ku shafi fuskokinkuda hannayenku, (tareda gwuiwar hannaye). Haƙiƙa Ubangiji ya tabbata mai afuwa mai gafara.

(YAHUDU DA AYYUKANSU)

44. Shin bakayi duba ba izuwa wad̄anda aka basu rabo na daga Littafi ba? Sune Yahudu) suna sayen ɓata dashiriya suna nufin ku bacewa hanyar (gaskiya, don ku zama kamar su). Allah ne mafi sani da magautanku, (ya baku Labari dasu donku nisance su) Allah ya isa mai kiyaye ku (d̄aga garesu) Allah ya isa mai tsare (ku daga kaidinsu).

1) Rangwame:.

وَاللَّهُ أَعْلَمُ بِأَعْدَآئِكُمْ وَكَفَىٰ بِاللَّهِ وَلِيّاً وَكَفَىٰ بِاللَّهِ
نَصِيراً ﴿44﴾ مِنَ الَّذِينَ هَادُواْ يُحَرِّفُونَ الْكَلِمَ عَن مَّوَاضِعِهِ
وَيَقُولُونَ سَمِعْنَا وَعَصَيْنَا وَاسْمَعْ غَيْرَ مُسْمَعٍ وَرَاعِنَا
لَيّاً بِأَلْسِنَتِهِمْ وَطَعْناً فِي الدِّينِ وَلَوْ أَنَّهُمْ قَالُواْ سَمِعْنَا وَأَطَعْنَا
وَاسْمَعْ وَانظُرْنَا لَكَانَ خَيْراً لَّهُمْ وَأَقْوَمَ وَلَكِن لَّعَنَهُمُ اللَّهُ
بِكُفْرِهِمْ فَلَا يُؤْمِنُونَ إِلَّا قَلِيلاً ﴿45﴾ * يَا أَيُّهَا الَّذِينَ أُوتُواْ ثمن
الْكِتَابَ ءَامِنُواْ بِمَا نَزَّلْنَا مُصَدِّقاً لِّمَا مَعَكُم مِّن قَبْلِ
أَن نَّطْمِسَ وُجُوهاً فَنَرُدَّهَا عَلَىٰ أَدْبَارِهَا أَوْ نَلْعَنَهُمْ
كَمَا لَعَنَّا أَصْحَابَ السَّبْتِ وَكَانَ أَمْرُ اللَّهِ مَفْعُولاً ﴿46﴾ إِنَّ اللَّهَ
لَا يَغْفِرُ أَن يُشْرَكَ بِهِ وَيَغْفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُ وَمَن
يُشْرِكْ بِاللَّهِ فَقَدِ افْتَرَىٰ إِثْماً عَظِيماً ﴿47﴾ أَلَمْ تَرَ إِلَى الَّذِينَ يُزَكُّونَ
أَنفُسَهُم بَلِ اللَّهُ يُزَكِّي مَن يَشَآءُ وَلَا يُظْلَمُونَ فَتِيلاً ﴿48﴾ انظُرْ كَيْفَ
يَفْتَرُونَ عَلَى اللَّهِ الْكَذِبَ وَكَفَىٰ بِهِ إِثْماً مُّبِيناً ﴿49﴾ أَلَمْ تَرَ إِلَى الَّذِينَ
أُوتُواْ نَصِيباً مِّنَ الْكِتَابِ يُؤْمِنُونَ بِالْجِبْتِ وَالطَّاغُوتِ
وَيَقُولُونَ لِلَّذِينَ كَفَرُواْ هَٰؤُلَآءِ أَهْدَىٰ مِنَ الَّذِينَ ءَامَنُواْ سَبِيلاً ﴿50﴾

45. Akwai daga Yahudawa mutanen dake jirkita kalmomi (wađanda Allah ya saukar a cikin Attaura sune kamannin Annabi Sallallahu alaihi wasallama) daga wurarensu, suna fađi (ga Annabi Sallalallahu alaihi wasallama idan ya umarce su da wani abu) "Munji (maganarka) mun sabawa (umarninka) ji ba abin ji (ai kar Allah yasa kaji, wato ka kurumce ko ka mutu." suna cewa): "Yi mana wauta don karkatarwa ga harasansu da suka cikin Addinin (Musulunci, da haƙiƙa su sunce "Munji, munbi, jimu, dubo mu," daya kasance mafi amfani a garesu kuma mafi adalci (maimakon kalmar RA'INA). Sai dai Allah ya tsine masu albarkane ya nisanta sune ga barin rahama tasa saboda kafircinsu, to, basa bada gaskiya sai kađan, (Abdullahi Ibn Salam da abokansa suna daga cikinsu) wađanda suka bada gaskiya).

(BAN TSORO DA NARKO GA AHA-LUL - KITABI)DA KIRAN AMERICA IZUWA ADDININ MUSLUMCT DA AUKUWAR DAMSI DA MASKHI WANDA ALLAH YA LABARTA AUKUWARSA GABAN TASHIN ƘIYAMA

46. Ya wađannan da aka basu Littafi! ku bada gaskiyaga abinda muka saukar (na Kur'ani) mai gasgatawa ga abinda ke taredaku ,(na daga Attaura) tun gaban bamu shafe fuskoki ba, (daga ido da hanci da gira,) mu mayar da ita a bisa bayayyakinta, (ta zama kamar ƙeya, wato allo đaya) ko mu mayar dasu birrai kamar yadda muka shafe ma'abota Asabar daga garesu, al'amarin Allah ya kasance abin aikatawa[1].

(ABINDA ALLAH YAKE GAFARTAWA)

47. Haƙiƙa Ubangiji baya gafarta shirka dashi, yana gafarta koma bayan wannan (daga zunubai) ga wanda yaga dama (ya shigar dashi aljanna bada azaba ba, wanda yaga dama yayi masa azabana daga mumunai sannan ya shigar dashi aljanna) wanda yayi shirka da Allah haƙiƙa ya ƙirƙiri zunubi mai girma.

(AHALUL - KITABI DA SAKAMAKONSU A KAN AYYUKANSU)

48. Shin bakayi duba ba ga wađanda suke tsarkake kawunansu? (Sune Yahudu suke cewa su "'ya" yan Allah ne kuma masoyansa) Haba'. Allah ne yake tsarkake wanda yaga dama (da imani) baza a zalunci kowa gwargwadon ɓawon đan balla [2] ba.

49. Yi mana ki! ƙaƙa suke ƙirƙirar ƙarya bisa Allah! Wannan ƙirƙira ya isa zunubi mabayyani. (Yayin da Ka'abu đan Lashrafu da makamantansa daga malaman Yahudu sukazo Makka, suka ga kasassun Badar, suka kwađaitar da mushrikai a kan đauko fansa dayaƙi da Annabi Sallahu alaihi wasallama sai Allah yace);

50. "Shin bakayi duba ba ga wađanda aka basu rabo na Littafi! suna bada gaskiya da Jibtu da Dagutu, (gumaka ne na ƙuraishu) suna fađa ga wađanda suka kafirta, (Abu Sufuyana da abokansa yayin da sukace dasu, 'Mune a kan gaskiya don mune ma'abuta đaki, mumuke shayar da al-hazai, mumuke đaukar fansa, ko kuwa shi Annabi Sallallahu alaihi wasallama alhali yabar addinin iyayensa ya yanke zumunta, yabar harami?) Ku wađannan; kune ma fiya shiriyar tafarki daga wađanda suka bada gaskiya".

1) Wannan Shine Damsin daya auku a wannan Shekara ta 1411 H. = 1991 m. indayahudawa (America) Suku dinga saka wasu tuskiki donsu Kare su daga t'iirmakin Saddam Husaini na Makamai Masu guba a yakin su da Saddam. Wanimn mu'ujiza ce ta AlƘur'ani mai bau mana ki da firgitarwa- - SsinaJy - Sheik Nasir Kabara.

2) Kodagon dabino.

أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَعَنَهُمُ ٱللَّهُۖ وَمَن يَلْعَنِ ٱللَّهُ فَلَن تَجِدَ لَهُۥ نَصِيرًا ﴿51﴾
أَمْ لَهُمْ نَصِيبٌ مِّنَ ٱلْمُلْكِ فَإِذًا لَّا يُؤْتُونَ ٱلنَّاسَ نَقِيرًا ﴿52﴾
أَمْ يَحْسُدُونَ ٱلنَّاسَ عَلَىٰ مَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦۖ فَقَدْ ءَاتَيْنَآ
ءَالَ إِبْرَٰهِيمَ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحِكْمَةَ وَءَاتَيْنَٰهُم مُّلْكًا عَظِيمًا ﴿53﴾
فَمِنْهُم مَّنْ ءَامَنَ بِهِۦ وَمِنْهُم مَّن صَدَّ عَنْهُۚ وَكَفَىٰ بِجَهَنَّمَ سَعِيرًا ﴿54﴾
إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِنَا سَوْفَ نُصْلِيهِمْ نَارًا كُلَّمَا نَضِجَتْ جُلُودُهُم
بَدَّلْنَٰهُمْ جُلُودًا غَيْرَهَا لِيَذُوقُواْ ٱلْعَذَابَۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَزِيزًا
حَكِيمًا ﴿55﴾ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَنُدْخِلُهُمْ جَنَّٰتٍ تَجْرِي
مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًاۖ لَّهُمْ فِيهَآ أَزْوَٰجٌ مُّطَهَّرَةٌ
وَنُدْخِلُهُمْ ظِلًّا ظَلِيلًا ﴿56﴾ ۞ إِنَّ ٱللَّهَ يَأْمُرُكُمْ أَن تُؤَدُّواْ
ٱلْأَمَٰنَٰتِ إِلَىٰٓ أَهْلِهَا وَإِذَا حَكَمْتُم بَيْنَ ٱلنَّاسِ أَن تَحْكُمُواْ بِٱلْعَدْلِۚ
إِنَّ ٱللَّهَ نِعِمَّا يَعِظُكُم بِهِۦٓۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ سَمِيعًا بَصِيرًا ﴿57﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ وَأُوْلِي ٱلْأَمْرِ مِنكُمْۖ
فَإِن تَنَٰزَعْتُمْ فِي شَيْءٍ فَرُدُّوهُ إِلَى ٱللَّهِ وَٱلرَّسُولِ إِن كُنتُمْ
تُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْأٓخِرِۚ ذَٰلِكَ خَيْرٌ وَأَحْسَنُ تَأْوِيلًا ﴿58﴾

ربع

51. Wađannan sune wađanda Allah ya tsine musu albarka. Wanda Allah ya tsine masa albarka, bazaka sami mai taimako a gareshi ba.
52. Shin suna da rabo ne na mulki? Bari! basu da komai dasuna dashi to, a wannan Lokaci bazasu ba mutane gwargwadon cibiyar đan balle ba.
53. Kai' shin suna yiwa Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) hassada ne a kan abinda Allah ya bashi na daga falalar (annabci da yawan mata/ Suna cewa "Da Annabi ne daya shagala ga barin mata!)" to, haƙiƙa mun baiwa zuriyar Annabi Ibrahim'Alaihis-salamu' Littafi da hikima, (Annabci) mun basu mulki maigirma. (Annabi dawuriu yana da mace casa'in da tara, Annabi Sulaimanu kuma yana da mace dubu).
54. Akwai daga garesu wanda ya bada gaskiya da Annabi "Sallallahu alaihi wasallama' akwai daga garesu wanda ya bijire (bai bada gaskiya dashi ba). Jahannama ta isa azaba ga wanda bai bada gaskiya dashi ba.

(SAKAMAKON KAFIRCI DA LADAN IMANI)

55. Haƙiƙa wađanda suka kafirce da ayoyinmu da sannu zamu shigar dasu wuta, kodayaushe fatunsu suka ƙone zamu musanya musu wata ƙonanniyar (a mayar da ita izuwa halinta na farko) donsu đanđani azaba, haƙiƙa Ubangiji ya tabbata mabuwayi ba abinda yake gajiyar dashi) gwani (a cikin halitta).
56. Wađanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagari da sannu zamushigar dasu aljannatai da ƙoramu suke gudana a ƙarƙashinta madawwama a cikinta har abada, mataye tsarkaka (daga haila da dukkan ƙazanta) na garesu a cikinta zamu shigar dasu inuwa madawwamiyar inuwa (da ba rana a cikinta).

(SIYASA MAGAMIYAGA HUKUMOMIN MUSULUNCI)

57. Haƙiƙa Ubangiji yana umarninku ku bada amanoni izuwa ma'abutanta (Allah ya fađi wannan aya ne yayin da Sayyadina Ali yardar Allah ta tabbata annabi (Sallallahu alaihi wasallama) saiya Musulunta saboda haka mabuđin Ka'aba har yau yana hannun zuriyarsa) in zakuyi hukunci tsakanin mutane (yana umarninku) kuyi hukunci da adalci, haƙiƙa Ubangiji madalla abinda yake yi muku gargađi dashi (bayar da amana da adalci cikin hukunci,) haƙiƙa Ubangiji ya tabbata maiji mai gani.

(WAJIBCIN BIN ALLAH DA MA'AIKINSA DA MAJIBANTAN AL'AMURA IN SUNYI UMARNI DA DA A)

58. Yuku wađanda kuka bada gaskiya! kubi Allah da ma'aikinsa da ma'abuta al'amura daga gareku (Hulafa'ur'rashidina. da shugabannin mazhabobi hudu, da alƙalai. da mahukunta, in sunyi umarni da đa'ar Allah da manzonsa) to in kunyi jayayya a cikin wani abu, to ku mayar dashi izuwa Allah (wato Alƙur'ani) da manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) muddar yana da rai. bayan ransa kuma amayar izuwa sunnansa in kun kasance kun bada gaskiya da Allah da ranar Lahira, wancananka (mayarwa izuwa garesu) shi yafi amfani (gareku daga jayayya da bin ra'ayi,) shi yafi kyakkyawar makoma.

أَلَمْ تَرَ إِلَى اَ۬لذِينَ يَزْعُمُونَ أَنَّهُمُۥٓ ءَامَنُواْ بِمَآ أُنزِلَ
إِلَيْكَ وَمَآ أُنزِلَ مِن قَبْلِكَ يُرِيدُونَ أَنْ يَّتَحَاكَمُوٓاْ
إِلَى اَ۬لطَّٰغُوتِ وَقَدُ اُمِرُوٓاْ أَنْ يَّكْفُرُواْ بِهِۦ وَيُرِيدُ
اُ۬لشَّيْطَٰنُ أَنْ يُّضِلَّهُمْ ضَلَٰلَۢا بَعِيداً ﴿59﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ تَعَالَوْاْ
إِلَىٰ مَآ أَنزَلَ اَ۬للَّهُ وَإِلَى اَ۬لرَّسُولِ رَأَيْتَ اَ۬لْمُنَٰفِقِينَ
يَصُدُّونَ عَنكَ صُدُوداً ﴿60﴾ فَكَيْفَ إِذَآ أَصَٰبَتْهُم مُّصِيبَةُۢ
بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ ثُمَّ جَآءُوكَ يَحْلِفُونَ بِاللَّهِ إِنْ أَرَدْنَآ
إِلَّآ إِحْسَٰناً وَتَوْفِيقاً ﴿61﴾ أُوْلَٰٓئِكَ اَ۬لذِينَ يَعْلَمُ اُ۬للَّهُ مَا فِي قُلُوبِهِمْ
فَأَعْرِضْ عَنْهُمْ وَعِظْهُمْ وَقُل لَّهُمْ فِيٓ أَنفُسِهِمْ
قَوْلَۢا بَلِيغاً ﴿62﴾ * وَمَآ أَرْسَلْنَا مِن رَّسُولٍ اِلَّا لِيُطَاعَ
بِإِذْنِ اِ۬للَّهِ وَلَوَ اَنَّهُمُۥٓ إِذ ظَّلَمُوٓاْ أَنفُسَهُمْ
جَآءُوكَ فَاسْتَغْفَرُواْ اُ۬للَّهَ وَاسْتَغْفَرَ لَهُمُ اُ۬لرَّسُولُ
لَوَجَدُواْ اُ۬للَّهَ تَوَّاباً رَّحِيماً ﴿63﴾ فَلَا وَرَبِّكَ لَا يُؤْمِنُونَ
حَتَّىٰ يُحَكِّمُوكَ فِيمَا شَجَرَ بَيْنَهُمْ ثُمَّ لَا يَجِدُواْ
فِيٓ أَنفُسِهِمْ حَرَجاً مِّمَّا قَضَيْتَ وَيُسَلِّمُواْ تَسْلِيماً ﴿64﴾

ثمن

(MUNAFUKAI DA AYYUKANSU)

59. (Ubangiji ya faɗi wannan aya mai zuwa yayin da wani Bayahude yayi husuma da wani munafiki, munafikin yace "a kai ƙara wurin ka'abu ɗan Lashrafu, bayahude yace a kai ƙara wajen Annabi (Sallallahu aiaihi wasallama,) sukaje wajen sa, sai yayi gaskiya sai manzon Allah ya baiwa bayahude gaskiya sai munufiki yace bai yarda ba, sukazo wajen Sayyidina Umaru, Bayahude yagaya masa wannan Lamari, sai Sayyadina Umaru ya tambayi munafiki yace "haka aka yi'?" Sai munakifi yace "i" sai Sayyidina Umaru ya kashe shi) Shin bakai duba ba izuwa waɗanda suke riyawa cewa haƙiƙa su sun bada gaskiya da abinda aka saukar a gareka, da abinda aka saukar daga gabanka? Suna nufin su kai ƙara izuwa tsagera (wato ka' abu ɗan -lashrafu alhali an umarcesu su kafirce dashi, Shaiɗan kuma yanaso ya ɓatar dasu ɓata mai nisa (ga barin gaskiya),

60. Idan ance dasu "Kuzo izuwa abinda Allah ya saukar (a cikin Al-ƙur'ani) kuma izuwa manzon Allah (don yayi hukunci tsakaninku.)" sai kaga munafikai suna bijirewa ga barin ka bujerewa.

61. Yaya zasuyi idan musibata same su, saboda abinda hannunsu ta gabatar (na daga kafirci da saɓo?) Sannan sukazo maka suna rantsuwa da Allah, "Bamu nufi komai dakai ƙaran nan izuwa waninka ba sai kyautatawa da daidaitawa (tsakanin maƙaraya guda biyu, ba muyi haka don gujewa gaskiya ba).

62. Waɗancananka ne waɗanda Allah yasan abinda yake zukatansu, (na daga munafunci da ƙarya a cikin hanzari,) to, rabu dasu kayi musu gargaɗi ka gaya musu magana mai tasiri a cikin zukatansu.

MASHARU IYATI TA WASSULI BIHI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA, UMAR NI AKAMA KAFA DASHI ALLAH TSIRA DA AMINCINN SU TABBATA AGARESHI DA SAURAN SU

63. Bamu aiko wani manzo ba sai don a bishi (a cikin abinda yayi umarni dashi ko yayi hani) da izinin Ubangiji. ba don a saɓe shi bada cewa su zamanin da suka zalunci kawunansu (dakai ƙara izuwa tsageran nan) sun zo maka suna masu tubasun nemi gafarar Allah, manzon Allah kuma ya nema musu gafara, to, dasun sami Allah mai karɓar tuba (a garesu) mai jinƙai.

64. To, haƙiƙa na rantse da Ubangijinka bazasu bada gaskiyaba sai sun sarautaka a cikin abinda ya rikice tsakaninsu, sannan bazasu sami ƙunci a cikin kawunansu daga abinda ka hukunta dashi basu jawu-jawuwa.

(BAYANIN DABI'O'IN MUTANE CIKIN BIN UMARNIN ADDININ UBANGIJI)

وَلَوْ أَنَّا كَتَبْنَا عَلَيْهِمُۥٓ أَنُ اقْتُلُوٓاْ أَنفُسَكُمُۥٓ أَوُ اخْرُجُواْ مِن
دِيَٰرِكُم مَّا فَعَلُوهُ إِلَّا قَلِيلٌ مِّنْهُمْ وَلَوْ أَنَّهُمْ فَعَلُواْ مَا يُوعَظُونَ
بِهِۦ لَكَانَ خَيْراً لَّهُمْ وَأَشَدَّ تَثْبِيتاً ﴿65﴾ وَإِذاً لَّأٓتَيْنَٰهُم
مِّن لَّدُنَّآ أَجْراً عَظِيماً ﴿66﴾ وَلَهَدَيْنَٰهُمْ صِرَٰطاً مُّسْتَقِيماً ﴿67﴾
وَمَنْ يُّطِعِ اِ۬للَّهَ وَالرَّسُولَ فَأُوْلَٰٓئِكَ مَعَ اَ۬لذِينَ أَنْعَمَ اَ۬للَّهُ
عَلَيْهِم مِّنَ اَ۬لنَّبِيٓـِٔينَ وَالصِّدِّيقِينَ وَالشُّهَدَآءِ وَالصَّٰلِحِينَ
وَحَسُنَ أُوْلَٰٓئِكَ رَفِيقاً ﴿68﴾ ذَٰلِكَ اَ۬لْفَضْلُ مِنَ اَ۬للَّهِ
وَكَفَيٰ بِاللَّهِ عَلِيماً ﴿69﴾ يَٰٓأَيُّهَا اَ۬لذِينَ ءَامَنُواْ خُذُواْ حِذْرَكُمْ
فَانفِرُواْ ثُبَاتٍ اَوِ انفِرُواْ جَمِيعاً ﴿70﴾ وَإِنَّ مِنكُمْ لَمَن
لَّيُبَطِّئَنَّ فَإِنْ أَصَٰبَتْكُم مُّصِيبَةٌ قَالَ قَدْ أَنْعَمَ اَ۬للَّهُ عَلَيَّ
إِذْ لَمْ أَكُن مَّعَهُمْ شَهِيداً ﴿71﴾ وَلَئِنْ أَصَٰبَكُمْ فَضْلٌ
مِّنَ اَ۬للَّهِ لَيَقُولَنَّ كَأَن لَّمْ يَكُنۢ بَيْنَكُمْ وَبَيْنَهُۥ مَوَدَّةٌ يَٰلَيْتَنِي كُنتُ
مَعَهُمْ فَأَفُوزَ فَوْزاً عَظِيماً ﴿72﴾ ۞ فَلْيُقَٰتِلْ فِي سَبِيلِ اِ۬للَّهِ
اِ۬لذِينَ يَشْرُونَ اَ۬لْحَيَوٰةَ اَ۬لدُّنْيَا بِالْأٓخِرَةِ وَمَنْ يُّقَٰتِلْ
فِي سَبِيلِ اِ۬للَّهِ فَيُقْتَلْ أَوْ يَغْلِبْ فَسَوْفَ نُؤْتِيهِ أَجْراً عَظِيماً ﴿73﴾

ربع

65. Da cewa mu haƙiƙa mun rubuta a garesu, ku kashe kanku, koku fita daga gidaddajinku (tamfar da mukayi ga Bani'isra'ila,) bazasu aikata shiba sai kaɗan daga garesu. da haƙiƙa suna ikata abinda ake musu gargadi dashi (na ɗa'a,) daya kasance mafi amfani garesu, mafi tsananin tabbatarwa (ga imaninsu).
66/67. Kuma yayin nan da mun basu Lada mai girma daga garemu, kuma da mun shiryesu tafarki madaidaici.

AL BISHIRINKU

68. (Yayin da ba'alin Sahabbai sukace da Annabi 'sallallahu alaihi wasallama' "Yaya zamu ganka a cikin aljanna kai kana cikin darajoji maɗaukaka?)" Sai Allah yace); "Wanda yabi Allah yabi manzonsa (cikin abinda yayi umarni dashi) to, waɗannan suna tareda waɗanda Allah yayi ni'ima a garesu, na daga Annabawa, da masu yawan ban gaskiya, da masu mutuwar shahada, da salihai, madalla waɗancananka abokan zama (a cikin aljanna!)".
69. Wancananka (shi) ne falala daga Allah, (wacce yayi musu alheri dashi, basu samu saboda ƙoƙarin ɗa'a ba) Allah ya isa masani (da sakamakon Lahira, ku amince da abinda yabaku Labari dashi).

(SIYASAR YAƘI A CIKIN MUSULUNCI WATO DABARUNSA)

70. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! ku riƙi tsarin ku (daga magautanku) ku zabura (izuwa yaƙinsu) ƙungiya bayan ƙungiyakoku zabura gaba ɗaya.
71. Akwai daga cikinku wanda Lallai yakan sanyayar da gwuiwa ga barin yaƙi (kamar Abdullahi ɗan Ubayyu munafiki da jama'arsa) to idan musibata same ku (kisa ko risɓawa) sai yace "Haƙiƙa Allah yayi ni'ima a gareni tunda ban kasance mahalarci taredasu ba".
72. Wallahi idan falala daga Allah ta same ku (buɗi ko ganima,) Lallai zai ce; "Ina ma na kasance taredasu in rabauta rabo mai girma," kamar babu wata soyayya tsakanin ku dashi.
73. To, waɗanda suke sayar da rayuwar duniya data Lahira suyi yaƙi a cikin inganta addinin Allah, yayi shahada ko yayi rinjaye da sannu zamu bashi Lada mai girma.

KWADAITARWA AKAN YAƘI DOMIN NEMAN SHAHADA

وَمَا لَكُمْ لَا تُقَٰتِلُونَ فِي سَبِيلِ اِ۬للَّهِ وَالْمُسْتَضْعَفِينَ مِنَ اَلرِّجَالِ
وَالنِّسَآءِ وَالْوِلْدَٰنِ اِ۬لذِينَ يَقُولُونَ رَبَّنَا أَخْرِجْنَا مِنْ هَٰذِهِ اِ۬لْقَرْيَةِ
اِ۬لظَّالِمِ أَهْلُهَا وَاجْعَل لَّنَا مِن لَّدُنكَ وَلِيّاً وَاجْعَل لَّنَا مِن لَّدُنكَ
نَصِيراً ﴿74﴾ اِ۬لذِينَ ءَامَنُواْ يُقَٰتِلُونَ فِي سَبِيلِ اِ۬للَّهِ وَالذِينَ كَفَرُواْ يُقَٰتِلُونَ
فِي سَبِيلِ اِ۬لطَّٰغُوتِ فَقَٰتِلُواْ أَوْلِيَآءَ اَلشَّيْطَٰنِ إِنَّ كَيْدَ اَلشَّيْطَٰنِ
كَانَ ضَعِيفاً ﴿75﴾ أَلَمْ تَرَ إِلَى اَلذِينَ قِيلَ لَهُمْ كُفُّواْ أَيْدِيَكُمْ
وَأَقِيمُواْ اُ۬لصَّلَوٰةَ وَءَاتُواْ اُ۬لزَّكَوٰةَ فَلَمَّا كُتِبَ عَلَيْهِمُ اُ۬لْقِتَالُ إِذَا فَرِيقٌ
مِّنْهُمْ يَخْشَوْنَ اَلنَّاسَ كَخَشْيَةِ اِ۬للَّهِ أَوْ أَشَدَّ خَشْيَةً وَقَالُواْ رَبَّنَا
لِمَ كَتَبْتَ عَلَيْنَا اَلْقِتَالَ لَوْلَا أَخَّرْتَنَا إِلَىٰ أَجَلٍ قَرِيبٍ قُلْ مَتَٰعُ اُ۬لدُّنْي۪ا
قَلِيلٌ وَالْأٓخِرَةُ خَيْرٌ لِّمَنِ اِ۪تَّق۪يٰ وَلَا تُظْلَمُونَ فَتِيلاً ﴿76﴾ * أَيْنَمَا تَكُونُواْ
يُدْرِككُّمُ اُ۬لْمَوْتُ وَلَوْ كُنتُمْ فِي بُرُوجٍ مُّشَيَّدَةٍ وَإِن تُصِبْهُمْ
حَسَنَةٌ يَقُولُواْ هَٰذِهِۦ مِنْ عِندِ اِ۬للَّهِ وَإِن تُصِبْهُمْ سَيِّئَةٌ يَقُولُواْ
هَٰذِهِۦ مِنْ عِندِكَ قُلْ كُلٌّ مِّنْ عِندِ اِ۬للَّهِ فَمَالِ هَٰؤُلَآءِ اِ۬لْقَوْمِ لَا يَكَادُونَ
يَفْقَهُونَ حَدِيثاً ﴿77﴾ مَّا أَصَابَكَ مِنْ حَسَنَةٍ فَمِنَ اَللَّهِ وَمَا أَصَابَكَ
مِن سَيِّئَةٍ فَمِن نَّفْسِكَ وَأَرْسَلْنَٰكَ لِلنَّاسِ رَسُولاً وَكَفَىٰ بِاللَّهِ شَهِيداً ﴿78﴾

ثمن

74. Meke gareku bazakuyi yaƙi a cikin inganta addinin Allah ba, da (kwato) raunana na maza da matada ƙananan yara, (waɗanda kafirai suka hana su hijira, suna cutar su, Ibin Abbas yardar Allah ta tabbata a garesu, yace "Nida gyatumata muna daga cikinsu)" waɗanda suke cewa "Ya Ubangijinmu fitar damu daga wannan alƙarya (Makka), wacce mutanenta suke azzalumai (saboda kafirci)" ka sanya mana majibincin al'amari daga gareka, ka sanya mana mai taimako daga gareka. (Haƙiƙa Allah ya amsa add'arsu ya sawwaƙe wa waɗansu fita, waɗansu suka wanzu har aka buɗe Makka. Annabi 'Sallallahu alaihi wasallama' ya sarauta Attabu ɗan Asidu yana ɗan shekara goma sha takwas, ya tsaida adalci da gaskiya).

75. Waɗanda suka bada gaskiya suna yaƙi a cikin inganta addinln Allah, waɗanda suka kafirta suna yaƙi a cikin inganta turbar shaiɗan, to, ku yaƙi mataimaka shaiɗan (kwa rinjaye su da ƙarfin Allah,) haƙiƙa kaidin shaiɗan (da muminai ya kasance rarrauna ne (bazai iya gware da kaidin Allah da kafirai ba) [1]. Bazai iya karewa daga uƙubar Allah akan kafirai ba. wane shi.

(SASHIN MASU RAGUWAR ZUCIYA)

76. Shin bakayi duba ba izuwa waɗannan da akace dasu "Ku kame hannayenku (ga barin yaƙi da kafirai" saboda cutar da kafirai suke musuba ? Waɗansu jama'a ne na Sahabbai) kuma ku tsayar da salla ku bada zakka, to yayin da aka wajabta yaƙi a garesu, sai ga waɗansu jama'a daga cikinsu suna tsoron mutuwa kamar tsoronsu da (azabar) Allah, ko mafi tsananin tsoro (daga haka) sukace don tsoron mutuwa "Ya Ubangijinmu, donme ka wajabta yaƙi a kanmu, donme baka jinkirta mana izuwa ajali makusanci ba?" Cenc (dasu) "Jin daɗin duniya ɗan ƙanƙani ne, aljanna tafi ga wanda yake jin tsoron Allah, baza a zalunce ku gwargwadon ɗan ɓalla ba,

77. Inda duk kuka kasance mutuwa zata riske ku, koda kun kasance a birane ababan ɗaukakawa (to, kada kuyi tsoron yaƙi don tsoron mutuwa,) idan daɗi ya same ku, (Yahudawa) sai suce "Wannan daga Allah yake" idan rashin daɗi ya same su, (tari da bala'i tamkar yadda ya faru garesu yayin da Annabi "Sallallahu alaihi wasallama' yaje Madina). sai suce "Wannan daga gareka ne" (wato shu'uminka ne) cene (dasu) "Kowanne (na daga daɗi wuya) daga Allah yake" to. meye ga waɗannan mutane basa kusan su fahimci abinda ake faɗa musu?.

78. Duk abinda ya same ka na daɗi to daga Allah ne, duk abinda ya same ka na wuya to daga kanka ne, mun aiko ka manzo ga dukkan al'umma, Allah ya isa shaida (a kan manzoncinka).

l) Bazai iya Karewa daga ukubar allah akan kafirai ba, waneshi!

مَّنْ يُّطِعِ الرَّسُولَ فَقَدْ أَطَاعَ اللَّهَ وَمَن تَوَلَّىٰ فَمَا أَرْسَلْنَٰكَ
عَلَيْهِمْ حَفِيظاً ۝79 وَيَقُولُونَ طَاعَةٌ فَإِذَا بَرَزُواْ مِنْ
عِندِكَ بَيَّت طَّآئِفَةٌ مِّنْهُمْ غَيْرَ الذِے تَقُولُ وَاللَّهُ يَكْتُبُ
مَا يُبَيِّتُونَ فَأَعْرِضْ عَنْهُمْ وَتَوَكَّلْ عَلَى اللَّهِ وَكَفَىٰ بِاللَّهِ
وَكِيلاً ۝80 أَفَلَا يَتَدَبَّرُونَ الْقُرْءَانَ وَلَوْ كَانَ مِنْ عِندِ غَيْرِ اللَّهِ
لَوَجَدُواْ فِيهِ اخْتِلَافاً كَثِيراً ۝81 وَإِذَا جَآءَهُمْ أَمْرٌ مِّنَ الْأَمْنِ
أَوِ الْخَوْفِ أَذَاعُواْ بِهِۦ وَلَوْ رَدُّوهُ إِلَى الرَّسُولِ وَإِلَىٰٓ أُوْلِے الْأَمْرِ
مِنْهُمْ لَعَلِمَهُ الذِينَ يَسْتَنۢبِطُونَهُۥ مِنْهُمْ وَلَوْلَا فَضْلُ اللَّهِ عَلَيْكُمْ
وَرَحْمَتُهُۥ لَاتَّبَعْتُمُ الشَّيْطَٰنَ إِلَّا قَلِيلاً ۝82 فَقَٰتِلْ فِے سَبِيلِ اللَّهِ
لَا تُكَلَّفُ إِلَّا نَفْسَكَ وَحَرِّضِ الْمُؤْمِنِينَ عَسَى اللَّهُ أَن يَّكُفَّ
بَأْسَ الذِينَ كَفَرُواْ وَاللَّهُ أَشَدُّ بَأْساً وَأَشَدُّ تَنكِيلاً ۝83
مَّنْ يَّشْفَعْ شَفَٰعَةً حَسَنَةً يَكُن لَّهُۥ نَصِيبٌ مِّنْهَا
وَمَنْ يَّشْفَعْ شَفَٰعَةً سَيِّئَةً يَكُن لَّهُۥ كِفْلٌ مِّنْهَا
وَكَانَ اللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَےْءٍ مُّقِيتاً ۝84 وَإِذَا حُيِّيتُم بِتَحِيَّةٍ فَحَيُّواْ بِأَحْسَنَ
مِنْهَا أَوْ رُدُّوهَا إِنَّ اللَّهَ كَانَ عَلَىٰ كُلِّ شَےْءٍ حَسِيباً ۝85

(BIN MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA BIN ALLAH NE)

79. Wanda yabi manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) haƙiƙa yabi Allah, wanda ya bada baya to, bamu aiko ka mai kiwo (ga aikinsu) ba.

80. (Munafukai) suna faɗa (gareka idan sunzo wajenka, "Al'amarinmu) biyayya a gareka" idan sun fita daga wurinka, waɗansu jama'a daga garesu saisu ƙulle wanin abinda suke fada (maka a kan idonka na biyayya saisu saɓa masa) Allah yana umarni da rubuce abin nan dasuke ƙullewa (a zukatansu don sakamako) to, ka rabu dasu kayi musu afuwa ka dogara ga Allah, Allah ya isa abin dogaro (a gareshi).

(LURA DA ALƘUR'ANI)

81. Shin basa Lura da al-ƙur'ani bane? (na daga abinda yake cikinsa na ƙaye), daya kasance daga wanin Allah dasun sami saɓani mai yawa a cikinsa.

(GANGANIMA A KAN LABARU)

82. Idan wani al'amari ya zo musu (da ga ƙungiyoyin Annabi 'Sallallahu alaihi sallama') na daga aminci (nasara) ko tsoro (risɓawa) saisu kwanzama shi (don zukatan muminai suyi rauni Manzon Allah Sallallahu ulaihi wasallama' ya cutu) sun maida wannan lamari izuwa Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallam) da kuma izuwa ma'abota ra'ayi a cikinsu (wato manyan Sahabbai) da waɗanda suke istinbaɗinsa da (ai masu binciken haƙiƙar yarda abin yake) da sunsanshi daga cikin su; ba don falalar Allah gareku (da Musulunci) bada rahama tasa (da Alƙur'ani) da kunbi shaiɗan, sai kaɗan.

(KWADAITARWA BISA YAƘI)

83. Sai kayi yaƙi ya Muhammadu (Sallallahu alaihi wasallama) a cikin inganta addinin Ubangiji ba a ɗora maka nauyin kowa ba sai kanka, (wato yi yaƙi kodakai kaɗai, haƙiƙa kai anyi maka al-ƙawari da nasara) ka kwaɗaitar da muminai (a kan yaƙi,) ana kaunar Ubangiji ya kame yaƙin waɗanda suka kafirta, Allah mafi tsananin yaƙi ne daga garesu, mafi tsananm ban kashi. (Sai Manzon Allah "Sallallahu alaihi wasallama yace "Na rantse da sarkin da raina take wurinsa, wallahi zan fita kodani kaɗai ne." Saiya fita da mutum saba'in izuwa Badar ƙarama, sai Allah yajefa razani a cikin zukatan kafirai basu fito ba).

FALALAR CETO DAGA MAN YAN MUTANE [1]

84. Wanda yai ceto (tsakanin mutane) ceto kyakkyawa (mai dacewa da shari'a), Ladaya kasance gareshi saboda ceton wanda yayi ceto mummunan (mai saɓa shari'a), rabo zai kasance gareshi saboda mummunan ceton. Ubangiji ya tabbata mai ƙarfin iko a kan komai, (saboda haka yake sada kowa da arzikinsa).

(SALLAMA DA AMSUWARTA)

85. Idan an gaishekuda gaisuwa (Assalamu alaikum) to ku gaida mai gaishekuda mafi kyau daga gareta. (kuce; Alaikumu-salamu-wa-Rahamatullahi-wa Barakatuhu), ku maida ita daidai dayadda akayi muku, (kuce "Alaikumus salamu)" haƙiƙa Ubangiji ya tabbata mai ƙididdige komai.

1) Misalin mutum yayi laifi ga babansa ya nemi ceto daga wan ubansa ko ƙanin ubansa ko mal amin ubansa. - Sanajy

حزب

۞ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ لَيَجْمَعَنَّكُمْ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ لَا رَيْبَ فِيهِ
وَمَنْ أَصْدَقُ مِنَ ٱللَّهِ حَدِيثًا ﴿86﴾ فَمَا لَكُمْ فِي ٱلْمُنَٰفِقِينَ فِئَتَيْنِ
وَٱللَّهُ أَرْكَسَهُم بِمَا كَسَبُوٓاْ أَتُرِيدُونَ أَن تَهْدُواْ مَنْ أَضَلَّ ٱللَّهُ
وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ فَلَن تَجِدَ لَهُۥ سَبِيلًا ﴿87﴾ وَدُّواْ لَوْ تَكْفُرُونَ
كَمَا كَفَرُواْ فَتَكُونُونَ سَوَآءً فَلَا تَتَّخِذُواْ مِنْهُمْ أَوْلِيَآءَ حَتَّىٰ
يُهَاجِرُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَإِن تَوَلَّوْاْ فَخُذُوهُمْ وَٱقْتُلُوهُمْ حَيْثُ
وَجَدتُّمُوهُمْ وَلَا تَتَّخِذُواْ مِنْهُمْ وَلِيًّا وَلَا نَصِيرًا ﴿88﴾
إِلَّا ٱلَّذِينَ يَصِلُونَ إِلَىٰ قَوْمِۭ بَيْنَكُمْ وَبَيْنَهُم مِّيثَٰقٌ
أَوْ جَآءُوكُمْ حَصِرَتْ صُدُورُهُمْ أَن يُقَٰتِلُوكُمْ أَوْ يُقَٰتِلُواْ
قَوْمَهُمْ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ لَسَلَّطَهُمْ عَلَيْكُمْ فَلَقَٰتَلُوكُمْ
فَإِنِ ٱعْتَزَلُوكُمْ فَلَمْ يُقَٰتِلُوكُمْ وَأَلْقَوْاْ إِلَيْكُمُ ٱلسَّلَمَ فَمَا جَعَلَ
ٱللَّهُ لَكُمْ عَلَيْهِمْ سَبِيلًا ﴿89﴾ سَتَجِدُونَ ءَاخَرِينَ يُرِيدُونَ أَن يَأْمَنُوكُمْ
وَيَأْمَنُواْ قَوْمَهُمْ كُلَّ مَا رُدُّوٓاْ إِلَى ٱلْفِتْنَةِ أُرْكِسُواْ فِيهَا فَإِن لَّمْ يَعْتَزِلُوكُمْ
وَيُلْقُوٓاْ إِلَيْكُمُ ٱلسَّلَمَ وَيَكُفُّوٓاْ أَيْدِيَهُمْ فَخُذُوهُمْ وَٱقْتُلُوهُمْ
حَيْثُ ثَقِفْتُمُوهُمْ وَأُوْلَٰٓئِكُمْ جَعَلْنَا لَكُمْ عَلَيْهِمْ سُلْطَٰنًا مُّبِينًا ﴿90﴾

86. Ubangiji Allah ba abin bautawa da gaskiya sai shi. Wallahai zai tadaku, ga kaɓurburanku a cikin ranar Al-ƙiyama ba kwankwanto a cikinta. Ba mafi gaskiyar zance daga Allah.

87. Menene sha'aninku kuka zama jama'a biyu a cikin munafikai? Ubangiji saboda abinda suka aikata na kafirci da sabo ya dankwafar dasu ga barin yaƙi basuci gaba ba, kuna neman ku shiryi wanda Allah ya ɓatar dashi! Duk wanda Allah ya ɓatar dashi! bazaka sami hanya ta shiriyagareshi ba.

88. Suna burin kafirtar ku tamfar da suka kafirta ku zama kudasu daidai a cikin kafirci kadaku ,riƙi masoya daga cikinsu sai sun ƙaurato fisabilillahi, ƙaura ingantacciya da take tabbatar da imaninsu idan suka bada baya kan abinda suke kai, to, sai ku kame su da ribacewa, ku kashesu inda duk kuka same su, kadaku ,riƙi wani abin jiɓinta daga cikinsu wala mataimaki da zakuyi taimako dashi a kan magautanku.

89. Sai waɗannan dasuke fakewa izuwa wasu mutane tsakaninsu daku akwai al-ƙawari na amana tasu amana garesu da wanda ya sadu izuwa garesu (kamar yadda Annabi yayi al-ƙawari da Hilalu ɗan Uwaimiru Ba'aslami Allah yayi yarda gareshi) ko waɗannan da sukazo muku alhali ƙirajensu sun ƙuntata ga barinsu yake ku tareda mutanen ka to, kadaku ,kula dasu da kisa ko damƙa. to, wannan da abinda ke bayansa an shafe shi da ayar kansakali da Allah ya nufa daya sallaɗa su a kanku shine yaƙarfafa zukatansu dasu yaƙe ku. sai dai shi bai so wannan ba saiya jefa razana a cikin zukatansu idan suka janye muku basu yaƙeku ba basu miƙa jawuwa izuwa gareku ba to, Allah bai sanya wata hanyagareku a kansu cafka da cashewa ba.

90. Da sannu zaka sami waɗansu mutane dasuke nufin su amintar daku wato su bayyana imani taredaku su amintar da mutanensu da kafirci, in sun koma izuwa garesu (sune asadu daga ɗafanu) duk sandaka maidasu izuwa fitina wato shirka saisu dankwata a cikinta. to in basu janye muku bada barin yaƙar ku. basu miƙa jawuwa izuwa gare kuba basu kame hannuwansu gabarin ku ba, to, ku danƙe su da ribacewa. ku kashe su inda duk kuka same su. Waɗancanenku mun sanya mukubin hanya hujja mabayyaniya a gareku a kansu (a kan kashe su da ribace su saboda yaudaraisu mummuna a kan mai kashewa).

وَمَا كَانَ لِمُؤْمِنٍ أَنْ يَّقْتُلَ مُؤْمِناً اِلَّا خَطَـٔاًۖ وَمَن قَتَلَ
مُؤْمِناً خَطَـٔاً فَتَحْرِيرُ رَقَبَةٍ مُّؤْمِنَةٍ وَدِيَةٌ مُّسَلَّمَةٌ اِلَىٰٓ
أَهْلِهِۦٓ إِلَّآ أَن يَّصَّدَّقُواْۖ فَإِن كَانَ مِن قَوْمٍ
عَدُوٍّ لَّكُمْ وَهْوَ مُؤْمِنٌ فَتَحْرِيرُ رَقَبَةٍ مُّؤْمِنَةٍۖ وَإِن
كَانَ مِن قَوْمٍ بَيْنَكُمْ وَبَيْنَهُم مِّيثَٰقٌ فَدِيَةٌ
مُّسَلَّمَةٌ اِلَىٰٓ أَهْلِهِۦ وَتَحْرِيرُ رَقَبَةٍ مُّؤْمِنَةٍۖ فَمَن
لَّمْ يَجِدْ فَصِيَامُ شَهْرَيْنِ مُتَتَابِعَيْنِ تَوْبَةً مِّنَ
اَ۬للَّهِۖ وَكَانَ اَ۬للَّهُ عَلِيماً حَكِيماًۖ (91) * وَمَن يَّقْتُلْ مُؤْمِناً ثمن
مُّتَعَمِّداً فَجَزَآؤُهُۥ جَهَنَّمُ خَٰلِداً فِيهَا وَغَضِبَ
اَ۬للَّهُ عَلَيْهِ وَلَعَنَهُۥ وَأَعَدَّ لَهُۥ عَذَاباً عَظِيماًۖ (92)
يَٰٓأَيُّهَا اَ۬لَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا ضَرَبْتُمْ فِي سَبِيلِ اِ۬للَّهِ فَتَبَيَّنُواْۖ
وَلَا تَقُولُواْ لِمَنْ أَلْقَىٰٓ إِلَيْكُمُ اُ۬لسَّلَٰمَ لَسْتَ مُؤْمِناً
تَبْتَغُونَ عَرَضَ اَ۬لْحَيَوٰةِ اِ۬لدُّنْيَا فَعِندَ اَ۬للَّهِ مَغَانِمُ
كَثِيرَةٌۖ كَذَٰلِكَ كُنتُم مِّن قَبْلُ فَمَنَّ اَ۬للَّهُ عَلَيْكُمْ
فَتَبَيَّنُوٓاْۖ إِنَّ اَ۬للَّهَ كَانَ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيراً (93)

91. Bai halatta ba ga mumini ya kashe Mumini a, saida kuskure wanda ya kashe mumini da kuskure. to ya "yanta wuyaye mumina bawa ko baiwa da diyya abar miƙawa izuwa ahalinsa sai inda sukai afuwa to idan abin kashewarnan ya kasance daga magautanku wato kafirai. Alhali shi muminine to sai a yanta wuyaye mumina (bawa ko baiwa) wanda bai sami wuyaye ba to, sai yayi azumin wata biyu majeranta, don tubadaga Allah, Ubangiji ya tabbata masani da halitta gwani cikin abinda ya shirya).

92. Wanda ya kashe mumini da gangan, sakamakonsa jahannamu mai dawwama a cikinta, kuma Allah yayi fushi dashi, ya tsine masa albarka, ya tanadi azaba maigirma a gareshi a cikin wuta.

(GARAJE A CIKIN HUKUNCI)

93. Yaku waɗanda suka bada gaskiya, idan kunyi tafiya saboda yaƙi, a cikin inganta addinin Allah, to, ku tafi sannu, kadaku ,fada ga wanda ya miƙa jawuwa izuwa gareku, kai ba mumini bane, kuna neman amfanin rayuwar duniya na ganima; ganimomi masu yawa na ga Ubangiji dazata wadatar daku ga buran kashe misalinsa don dukiyarsa hakanan kuka kasance tun gaba. ana kiyaye jininkuda dukiyoyinkuda zarar fadin shahada, to, Allah yai baiwa a garekuda shuhura da imani da daidaito kan tafarki, to, kuyi hankali kadaku ,kashe mumini. ku aikata ga mai shigowa cikin Musulunci kamar yadda aka aikata muku, haƙiƙa Ubangiji masanine da abinda kuke aikatawa.

(YAƘI FISABILILLAHI DA FALALARSA)

لَا يَسْتَوِي الْقَٰعِدُونَ مِنَ الْمُؤْمِنِينَ غَيْرَ أُولِي الضَّرَرِ وَالْمُجَٰهِدُونَ فِي سَبِيلِ
اللَّهِ بِأَمْوَالِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ فَضَّلَ اللَّهُ الْمُجَٰهِدِينَ بِأَمْوَالِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ
عَلَى الْقَٰعِدِينَ دَرَجَةً وَكُلًّا وَعَدَ اللَّهُ الْحُسْنَىٰ وَفَضَّلَ اللَّهُ الْمُجَٰهِدِينَ
عَلَى الْقَٰعِدِينَ أَجْرًا عَظِيمًا (94) دَرَجَٰتٍ مِّنْهُ وَمَغْفِرَةً وَرَحْمَةً وَكَانَ
اللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا (95) إِنَّ الَّذِينَ تَوَفَّىٰهُمُ الْمَلَٰٓئِكَةُ ظَالِمِي أَنفُسِهِمْ
قَالُوا فِيمَ كُنتُمْ قَالُوا كُنَّا مُسْتَضْعَفِينَ فِي الْأَرْضِ قَالُوا أَلَمْ تَكُنْ أَرْضُ
اللَّهِ وَاسِعَةً فَتُهَاجِرُوا فِيهَا فَأُولَٰٓئِكَ مَأْوَىٰهُمْ جَهَنَّمُ وَسَآءَتْ
مَصِيرًا (96) إِلَّا الْمُسْتَضْعَفِينَ مِنَ الرِّجَالِ وَالنِّسَآءِ وَالْوِلْدَٰنِ
لَا يَسْتَطِيعُونَ حِيلَةً وَلَا يَهْتَدُونَ سَبِيلًا (97) فَأُولَٰٓئِكَ عَسَى اللَّهُ
أَن يَعْفُوَ عَنْهُمْ وَكَانَ اللَّهُ عَفُوًّا غَفُورًا (98) * وَمَن يُهَاجِرْ فِي سَبِيلِ اللَّهِ ربع
يَجِدْ فِي الْأَرْضِ مُرَٰغَمًا كَثِيرًا وَسَعَةً وَمَن يَخْرُجْ مِنۢ بَيْتِهِۦ مُهَاجِرًا
إِلَى اللَّهِ وَرَسُولِهِۦ ثُمَّ يُدْرِكْهُ الْمَوْتُ فَقَدْ وَقَعَ أَجْرُهُۥ عَلَى اللَّهِ وَكَانَ
اللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا (99) وَإِذَا ضَرَبْتُمْ فِي الْأَرْضِ فَلَيْسَ عَلَيْكُمْ
جُنَاحٌ أَن تَقْصُرُوا مِنَ الصَّلَوٰةِ إِنْ خِفْتُمْ أَن يَفْتِنَكُمُ
الَّذِينَ كَفَرُوا إِنَّ الْكَٰفِرِينَ كَانُوا لَكُمْ عَدُوًّا مُّبِينًا (100)

94. Mazauna ga buran yaƙi na muminai bazasuyi daidai da masu yaƙi fisabilillahi ba, da dukiyoyinsu da kawunansu, sai ma'abota Lalura. Allah yafifita masu yaƙi da dukiyoyinsu da kawunansu a kan mazauna ga buran yaƙi saboda lalura, a cikin daraja kowanne daga jama'ar nan guda biyu Allah ya al-ƙawarta masa aljanna, yafifita mayaƙa a kan mazauna da Lada maigirma.
95. Darajoji daga Allah da rahama daga Allah, Ubangiji ya tabbata mai gafara mai jinƙai (ga ma'abuta ɗa'a).

(MASU HIJIRA SABODA ALLAH DA MASU JINKIRI GA BARIN HIJIRA)

(Waɗansu jama'a sun Musulunta basuyi Hijira ba aka kashe su a ranar badar tareda kafirai, sai Allah yace);
96. Waɗanda Mala'iku suka karɓi rawukansu suna masu zaluntar kawukansu, da zama tareda kafirai da barin hijira sukace dasu a cikin me kuka kasance. suka faɗa suna masu hanzari, "Mun kasance raunana a cikin ƙasar Makka, bamu sami damar tsaida addininmu ba" sai sukace dasu "Shin ƙasar Allah ba mayalwaciya bace?" To, kuyi hijjira a cikinta daga ƙasar kafirci izuwa waninsa, to, sai Ubangiji yace; To, waɗancanenka makomarsu jahannama, ta mugusta makoma!
97. Sai ko raunana na daga maza da matada ƙananan yara waɗanda basu sami damar wata dabara bakan hijira ba, basu sami shiriyar sanin hanyoyi izuwa ƙasar hijira ba.
98. To, waɗancananka ana ƙaunar Allah yayi musu rangwame, Ubangiji ya kasance mai afuwa mai gafara.

(YADDA AKE SALLA A CIKIN TAFIYA DAYAƘI DA SALLAR ƘASARU)

99. Wanda yayi hijira saboda Allah zai sami wurin hijira mai yawa dayalwa a cikin arziki, wanda yafita daga ɗakinsa yana mai hijira izuwa Allah da ma'aikinsa, sannan mutuwa ta riske shi a hanya (kamar Janda'u ɗan Lamrata Allais-salam) to haƙiƙa Ladansa ya auku a bisa Allah, Ubangiji ya kasance mai gafara mai rahama a gareshi.
100. Idan kunyi tafiya a cikin ƙasa babu Laifi a gareku kuyi ƙasaru a cikin salla (ku mayar da raka'a huɗu izuwa biyu,) in kunji tsoron kafirai su fitinanceku, (hakanamma ko bakuji tsoron fitina ba, tafiyar data kai mil arba'in da takwas) haƙiƙa kafirai sun kasance magauta mabayyanan ƙiyayya a gareku.

وإذا كنت فيهم فأقمت لهم الصلوة فلتقم طآئفة
منهم معك وليأخذوا أسلحتهم فإذا سجدوا فليكونوا
من ورآئكم ولتأت طآئفة اخرى لم يصلوا فليصلوا
معك وليأخذوا حذرهم وأسلحتهم ود الذين
كفروا لو تغفلون عن أسلحتكم وأمتعتكم فيميلون
عليكم ميلة واحدة ولا جناح عليكم إن كان
بكم أذى من مطر او كنتم مرضى أن تضعوا أسلحتكم
وخذوا حذركم إن الله أعد للكافرين عذابا مهينا ﴿101﴾
فإذا قضيتم الصلوة فاذكروا الله قياما
وقعودا وعلى جنوبكم فإذا اطمأننتم فأقيموا الصلوة
إن الصلوة كانت على المؤمنين كتابا موقوتا ﴿102﴾ ولا تهنوا
في ابتغآء القوم إن تكونوا تألمون فإنهم يألمون كما
تألمون وترجون من الله ما لا يرجون وكان الله عليما
حكيما ﴿103﴾ * إنا أنزلنا إليك الكتاب بالحق لتحكم
بين الناس بما أريك الله ولا تكن للخآئنين خصيما ﴿104﴾

ثمن

101. idan ka kasance a cikinsu ya Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) alhali kuna tsoron magauta, ka tsayar da salla garesu, to, wađansu daga cikinku su tsaya tareda kai, wađansu kuma su dakata, wađanda suka tsaya taredakai đin ,to, su riƙi makamansu taredasu, to, idan sukayi salla to su kasance a bayanku su kiyaye ku har ku gama sallarku, wađanda suka dakata basuyi salla ba, to, su zo suyi salla taredakai su riƙi tsarinsu da makamansu taredasu harsu ƙare sallar, (Annabi Sallallahu alaihi wasallama ya aikata wannan a bađani Nahlata, wuri ne) wađanda suka kafirta sun guraci ku rabkana ga barin makamanku, da kayayyakin shirye-shiryenku, to, su karkata a kanku karkata guda đaya, wato suyi đauki a kanku, saboda haka akace ku riƙi makami, babu Laifi a gareku idan akwai cuta a gareku, ta ruwa ko kuka kasance marasa Lafiya, ku ajiye makaminku, ku riƙi tsarinku, haƙiƙa Ubangiji ya tanadi azaba mai wulaƙantarwa ga kafirai.

(WURUDAI NA BAYAN SALLOLI DA WAJABCIN SALLA DA HARAMCIN JINKIRTA TA GA BURAN LOKACINTA)

102. To, idan kun gama salla, sai ku ambaci Allah. (da hailala. da tasbihi da waninsa.) a zaune,. ko a tsaye ko a kishingiđe, (wato a bisa kowane hali,) idan kun nutsu to, ku tsaida salla da haƙƙokinta, haƙiƙa salla ta kasance abar wajabtawa a kan muminai, abar yankawa Lokaci, ba ajinkirta ta ga buran Lokacinta.

(KWADAITARWA A KAN YAƘI)

(Annabi Sallallahu alaihi wasallama) ya aiki wađansu mutane don neman Abu Safiyana yayin da suka dawo daga Uhudu, sai sukayi ƙarar miyagun cikinsu. manzon Allah sallallahu alaihi wasallama yayi masa gafara Ya kuɓutar dashi, sai wannan aya ta sauka. Itace inna anzalnaka, sai Allah yace):

103. Kada kuyi rauni a cikin neman kafirai. in kun kasance kunajin rađađi to su ma suna jin rađađi tamfar da kuke ji, kuma kuna ƙaunar abinda basa ƙauna ga Allah, na daga nasara da saka mako,(kunƙaru akansu da wannan. yakamata ku kasance mafiya kwađayi daga garesu a cikinsa), Ubangiji ya tabbata masani da komai. gwani cikin aiki.

(KIYAYE HAƘUƘUWA DA RASHIN NUNA GÃTA A CIKIN HUKUNCE -HUKUNCE DA ƘABILANCI)

104. Haƙiƙa mu mun saukar da Littafi gareka da gaskiya. don kayi hukunci tsakanin mutane da abinda Allah yasanar dakai a cikinsa (đi imatu ya saci soke nan ga bayahude sai aka same ta nan gareshi sai di'imatu yace bayahude ne ya sace,. sai bayahude ya rantse). kadaka kasance mai hnsuma ga maha'inta (kamar đi'imatu).

وَاسْتَغْفِرِ اللَّهَ إِنَّ اللَّهَ كَانَ غَفُوراً رَّحِيماً ﴿105﴾ وَلَا تُجَادِلْ
عَنِ الَّذِينَ يَخْتَانُونَ أَنفُسَهُمْ إِنَّ اللَّهَ لَا يُحِبُّ مَن كَانَ خَوَّاناً
أَثِيماً ﴿106﴾ يَسْتَخْفُونَ مِنَ النَّاسِ وَلَا يَسْتَخْفُونَ مِنَ اللَّهِ
وَهُوَ مَعَهُمْ إِذْ يُبَيِّتُونَ مَا لَا يَرْضَىٰ مِنَ الْقَوْلِ وَكَانَ اللَّهُ
بِمَا يَعْمَلُونَ مُحِيطاً ﴿107﴾ هَٰأَنتُمْ هَٰؤُلَآءِ جَادَلْتُمْ عَنْهُمْ
فِي الْحَيَوٰةِ الدُّنْيَا فَمَن يُجَادِلُ اللَّهَ عَنْهُمْ يَوْمَ الْقِيَٰمَةِ
أَم مَّن يَكُونُ عَلَيْهِمْ وَكِيلاً ﴿108﴾ وَمَن يَعْمَلْ سُوٓءاً أَوْ يَظْلِمْ
نَفْسَهُۥ ثُمَّ يَسْتَغْفِرِ اللَّهَ يَجِدِ اللَّهَ غَفُوراً رَّحِيماً ﴿109﴾ وَمَن يَكْسِبْ
إِثْماً فَإِنَّمَا يَكْسِبُهُۥ عَلَىٰ نَفْسِهِۦ وَكَانَ اللَّهُ عَلِيماً حَكِيماً ﴿110﴾
وَمَن يَكْسِبْ خَطِيٓـَٔةً أَوْ إِثْماً ثُمَّ يَرْمِ بِهِۦ بَرِيٓـٔاً
فَقَدِ احْتَمَلَ بُهْتَٰناً وَإِثْماً مُّبِيناً ﴿111﴾ وَلَوْلَا فَضْلُ اللَّهِ
عَلَيْكَ وَرَحْمَتُهُۥ لَهَمَّت طَّآئِفَةٌ مِّنْهُمْ أَن يُضِلُّوكَ
وَمَا يُضِلُّونَ إِلَّآ أَنفُسَهُمْ وَمَا يَضُرُّونَكَ مِن شَيْءٍ
وَأَنزَلَ اللَّهُ عَلَيْكَ الْكِتَٰبَ وَالْحِكْمَةَ وَعَلَّمَكَ
مَا لَمْ تَكُن تَعْلَمُ وَكَانَ فَضْلُ اللَّهِ عَلَيْكَ عَظِيماً ﴿112﴾

105. Ka nemi gafarar Allah daga abinda kayi niyya, haƙiƙa Ubangiji ya tabbata mai gafara mai rahama.
106. Kada kayi jayayyaga barin waɗannan dasuke ha'intar kawukansu, haƙiƙa Ubangiji ba yasan wanda ya kasance mai ha'inci maiɗaukar alhaki.
107. Suna neman ɓuya don jin kunya daga mutane, amma basa neman ɓuya don Jin kunyar Allah, alhali shi yana taredasu zamanin da suka ƙudure abinda bai yarda dashi bana magana, shine rantsuwarsu a kan kore sata daga di'imatu da ɗafawa Bayahude ita, Ubangiji ya tabbata mai kewayewar sani da abinda suke aikatawa
108. To, yaku waɗannàn kunyi jayayyaga barin su (Di'imatu da mutanensa watau) kun yi musu ;yaƙi a rayuwar duniya,to, waye zai yaƙi Allah ga barinsu ranar Al-ƙiyama, ko kuwa waye zai zama wakili a kansu? Babu.
109. Wanda ya aikata Laifin (dazai ɗafa wa wani,) koya zalunci kansa, sannan ya nemi gafarar Allah, zai sami Allah mai gafara ne gareshi mai jinƙai.
110. Wanda ya aikata Laifi, to, ya aikata shi a kan kansa kawai, Ubangiji ya tabbata masani mai hikima.
111. Wanda ya aikata kuskure, (watau sagira ko kabira,) sannan ya ɗafawa waninshi, to, haƙiƙa ya girba ƙarya da zunubi mabayyani.
112. Badon falalar Allah gareka ba, da jinƙansa da kiyaye ka (ya Annabi sallallahu alaika wasallama), da waɗansu mutane daga cikinsu sun nufi su ɓashsheka ga barin hukunci da gaskiya, bazasu ɓatar da kowa ba sai kansu, bazasu cuce ka komai ba, Allah ya saukar da ƙur'ani a gareka da hukunce-hukunce, yasanar dakai abinda baka kasance ka sani bana hukunce-hukunce da Labarin gaibu, falalar Ubangiji ta kasance maigirma a gareka.

(HANI GA BARIN GANAWA DA SHARRI DA SAKAMAKON WANDA YA AIKATA ALHERI SABODA ALLAH)

ربع

۞ لَّا خَيْرَ فِي كَثِيرٍ مِّن نَّجْوَاهُمْ إِلَّا مَنْ أَمَرَ بِصَدَقَةٍ
أَوْ مَعْرُوفٍ أَوْ إِصْلَاحٍ بَيْنَ النَّاسِ وَمَن يَفْعَلْ
ذَٰلِكَ ابْتِغَاءَ مَرْضَاتِ اللَّهِ فَسَوْفَ نُؤْتِيهِ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿113﴾
وَمَن يُشَاقِقِ الرَّسُولَ مِن بَعْدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُ الْهُدَىٰ وَيَتَّبِعْ غَيْرَ
سَبِيلِ الْمُؤْمِنِينَ نُوَلِّهِ مَا تَوَلَّىٰ وَنُصْلِهِ جَهَنَّمَ وَسَاءَتْ
مَصِيرًا ﴿114﴾ إِنَّ اللَّهَ لَا يَغْفِرُ أَن يُشْرَكَ بِهِ وَيَغْفِرُ
مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَاءُ وَمَن يُشْرِكْ بِاللَّهِ فَقَدْ ضَلَّ ضَلَالًا
بَعِيدًا ﴿115﴾ إِن يَدْعُونَ مِن دُونِهِ إِلَّا إِنَاثًا وَإِن يَدْعُونَ
إِلَّا شَيْطَانًا مَّرِيدًا ﴿116﴾ لَّعَنَهُ اللَّهُ وَقَالَ لَأَتَّخِذَنَّ
مِنْ عِبَادِكَ نَصِيبًا مَّفْرُوضًا ﴿117﴾ وَلَأُضِلَّنَّهُمْ
وَلَأُمَنِّيَنَّهُمْ وَلَآمُرَنَّهُمْ فَلَيُبَتِّكُنَّ آذَانَ الْأَنْعَامِ
وَلَآمُرَنَّهُمْ فَلَيُغَيِّرُنَّ خَلْقَ اللَّهِ وَمَن يَتَّخِذِ الشَّيْطَانَ
وَلِيًّا مِّن دُونِ اللَّهِ فَقَدْ خَسِرَ خُسْرَانًا مُّبِينًا ﴿118﴾
يَعِدُهُمْ وَيُمَنِّيهِمْ وَمَا يَعِدُهُمُ الشَّيْطَانُ إِلَّا غُرُورًا ﴿119﴾
أُولَٰئِكَ مَأْوَاهُمْ جَهَنَّمُ وَلَا يَجِدُونَ عَنْهَا مَحِيصًا ﴿120﴾

113. Babu alheri a cikin yawaici daga ganawa da mutane, sai dai ganawa ta wanda yayi umarni da sadaka ko aikin alheri. ko gyara tsakanin mutane. wanda ya aikata wancananka abin ambato don neman yadar Allah da sannu zamu bashi Lada maigirma.

(HARAMCIN SABA IJMA'I)

114. Wanda ya sabawa Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) a cikin abinda yazo dashi bayan gaskiya ta bayyana gareshi da mu'ujizozi, yabi wata hanya daban bata muminai ba, ma.jibinta masa abinda yajiƃinta na daga ƃata, a nan duniya mu shigar dashi jahannama a Lahira, ta mugusta makoma.

(MUSHIRIKANCI DA HADARINSA DA SHAIƊAN DA FITINARSA) WATAU DA TSARIN KAFIRAI AYAU WANDA SUKE CEWA DASHI KONSU TUSHIN

115. Haƙiƙa Ubangiji baya gafarta ayi shirka dashi, yana gafarta koma bayan wancananka ga wanda yaga dama, wanda yayi shirka da Allah, to, haƙiƙa ya ƃata, ƃata mai nisa ga barin gaskiya.

116. Mushirikai basa bautawa Allah sai gumaka (kamar latada uzza da manata) basa bautawa komai sai mai taurin kai.

117. Allah ya tsine masa albarka, yace Wallahi zan sanya rabo abin kaddarawa daga bayinka ga kaina, (watau na kirawo su izuwa bautata.)

118. Lallai zan ƃatar dasu ga barin gaskiya da jefa wasuwasi, Lallai zan jefa gurin tsawon rai da musun al-ƙiyama a zuciyarsu, kuma Lallai zan umarce su, su dinga daddatsa kunnen dabbobi, (sun kuwa aikata wannan ɗin ga Ba-hira da Wasila, da Hami, nonon gumaka da bayan gumaka da uban maza.) Lallai zan umarce su, sujirkita halittar Allah, (wato addininsa da kafirci dahalatta abinda ya haramta, wannan aya fassararta ta bayyana sosai a cikin aikin da 'yan mulkin mallake sukayi a cikin al'ummar Musulunci), wanda ya riƙi shaiɗan uban ɗaki ba Allah ba, to, haƙiƙa ya taƃe, taƃewa mabayyaninya (kamar Musulmin duniya da suka mayar da Dasturin Turawa Al-ƙur'aninsu).

119. Yanayi musu al-ƙawarin tsawon rai, yana jefa su cikin gurace-gurace, (samun manya - manyan muƙamai da musun tashin Al-ƙiyama,) Shaiɗan bayayi musu al-ƙawarin komai sai ruɗi.

120. Waɗancananka makomarsu jahannama, bazasu sami maarɗaɗa ga barin ta ba.

ثمن

وَالَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ الصَّٰلِحَٰتِ سَنُدْخِلُهُمْ جَنَّٰتٖ
تَجْرِے مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا أَبَداٗ وَعْدَ اللَّهِ
حَقّاٗ وَمَنْ أَصْدَقُ مِنَ اللَّهِ قِيلاٗ ﴿121﴾ ۞ لَّيْسَ بِأَمَانِيِّكُمْ
وَلَا أَمَانِيِّ أَهْلِ الْكِتَٰبِ مَنْ يَّعْمَلْ سُوٓءاٗ يُجْزَ بِهِۦ
وَلَا يَجِدْ لَهُۥ مِن دُونِ اللَّهِ وَلِيّاٗ وَلَا نَصِيراٗ ﴿122﴾
وَمَنْ يَّعْمَلْ مِنَ الصَّٰلِحَٰتِ مِن ذَكَرٍ أَوْ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤْمِنٞ
فَأُوْلَٰٓئِكَ يَدْخُلُونَ الْجَنَّةَ وَلَا يُظْلَمُونَ نَقِيراٗ ﴿123﴾ وَمَنْ
أَحْسَنُ دِيناٗ مِّمَّنْ أَسْلَمَ وَجْهَهُۥ لِلَّهِ وَهُوَ مُحْسِنٞ وَاتَّبَعَ مِلَّةَ
إِبْرَٰهِيمَ حَنِيفاٗ وَاتَّخَذَ اللَّهُ إِبْرَٰهِيمَ خَلِيلاٗ ﴿124﴾ وَلِلَّهِ
مَا فِي السَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ وَكَانَ اللَّهُ
بِكُلِّ شَيْءٍ مُّحِيطاٗ ﴿125﴾ وَيَسْتَفْتُونَكَ فِي النِّسَآءِ قُلِ اللَّهُ
يُفْتِيكُمْ فِيهِنَّ وَمَا يُتْلَىٰ عَلَيْكُمْ فِي الْكِتَٰبِ فِي يَتَٰمَى النِّسَآءِ
الَّٰتِي لَا تُؤْتُونَهُنَّ مَا كُتِبَ لَهُنَّ وَتَرْغَبُونَ أَن تَنكِحُوهُنَّ
وَالْمُسْتَضْعَفِينَ مِنَ الْوِلْدَٰنِ وَأَن تَقُومُواْ لِلْيَتَٰمَىٰ بِالْقِسْطِ
وَمَا تَفْعَلُواْ مِنْ خَيْرٖ فَإِنَّ اللَّهَ كَانَ بِهِۦ عَلِيماٗ ﴿126﴾

121. Wađanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagari da sannu zamu shigar dasu aljannatai da ƙoramu suke kwarara daga ƙarƙashinta madawwama a cikinta har abada, Allah ya al-ƙawarta wannan al-ƙawartawa ya tabbatar dashi tabbatarwa, ba wanda yafi Allah gaskiyar magana.

(TSAMMANIN WARABBAKA DA SAKAMAKONSA)

122.Wannan Lamari ba gurace-guracenkune bako na Ahalil - Kita-bi, Lamari ya tabbata a cikin aiki nagari, wanda ya aikata mummunan aiki za a saka masa da mummunan sakamako a duniyako a Lahira (sakamakon duniya bala'i dajarrabu, na Lahira kuma shiga wuta, Allah ya kiyashemu amin,) bazai sami wani majibinci ba Allah ba, wala wani dazai hana masa azabar Allah.

123. Wanda ya aikata wani abu daga ayyuka nagari, na daga namiji ko mace, alhali yana mumini, to, wađancanenka suna shiga aljanna, baza a zalunce su ƙwayar komayyar bawan đan ɓalle ba.

(FALALAR KIRA IZUWA ALLAH)

124. Wanene mafi kyaun addini daga wanda ya jawu gabadayan-sa izuwa Ubangiji, alhali yana da cikakken kađaita Allah, kuma yabi addinin Annabi Ibrahima (Alaihissalamu) totar, Ubangiji ya riƙi Annabi Ibrahima (Alaihissalamu) badađi.

125. Mulkin abinda yake cikin sammai da ƙassai' naga Allah ne, (mallaka da halittada bauta,) Ubangiji ya tabbata mai kewayewa da sani da komai, (sani da iko.)

(HAƘƘUƘUWAN RAUNANA DA MAGANTAR RIKICE - RI KICE NA CIKIN GIDA)

126. Suna neman fatawar ka a cikin sha'anin matada gadonsu, Cene dasu Allah yanayi muku jawabi a cikinsu da abinda ake karantawa a gareku a cikin Alƙur'ani. a cikin marayun mata wađanda baku basu abinda aka rubuta a garesu na daga gado ba, kuna kuma ƙinku auresu saboda muninsu, kunayi musu ƙeta kadasuyi aure donku gaje su, to, kadaku ,kuma irin wanna. hakana kuma yanayi muku jawabi a cikin ƙananan yara ku basu haƙƙin su, yana kuma umartar ku ku tsaya da adalci ga marayu a cikin gado da sadaki, duk abinda zaku aikata na alheri to, haƙiƙa Allah ya tabbata masani dashi.

وَإِنِ امْرَأَةٌ خَافَتْ مِنْ بَعْلِهَا نُشُوزًا أَوْ إِعْرَاضًا
فَلَا جُنَاحَ عَلَيْهِمَا أَنْ يَصَّالَحَا بَيْنَهُمَا صُلْحًا وَالصُّلْحُ خَيْرٌ
وَأُحْضِرَتِ الْأَنْفُسُ الشُّحَّ وَإِنْ تُحْسِنُوا وَتَتَّقُوا فَإِنَّ اللَّهَ
كَانَ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرًا (127) وَلَنْ تَسْتَطِيعُوا أَنْ تَعْدِلُوا
بَيْنَ النِّسَاءِ وَلَوْ حَرَصْتُمْ فَلَا تَمِيلُوا كُلَّ الْمَيْلِ
فَتَذَرُوهَا كَالْمُعَلَّقَةِ وَإِنْ تُصْلِحُوا وَتَتَّقُوا فَإِنَّ اللَّهَ
كَانَ غَفُورًا رَحِيمًا (128) * وَإِنْ يَتَفَرَّقَا يُغْنِ اللَّهُ ربع
كُلًّا مِنْ سَعَتِهِ وَكَانَ اللَّهُ وَاسِعًا حَكِيمًا (129) وَلِلَّهِ
مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ وَلَقَدْ وَصَّيْنَا الَّذِينَ أُوتُوا الْكِتَابَ
مِنْ قَبْلِكُمْ وَإِيَّاكُمْ أَنِ اتَّقُوا اللَّهَ وَإِنْ تَكْفُرُوا فَإِنَّ لِلَّهِ
مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ وَكَانَ اللَّهُ غَنِيًّا حَمِيدًا (130)
وَلِلَّهِ مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ وَكَفَىٰ بِاللَّهِ وَكِيلًا (131)
إِنْ يَشَأْ يُذْهِبْكُمْ أَيُّهَا النَّاسُ وَيَأْتِ بِآخَرِينَ وَكَانَ اللَّهُ
عَلَىٰ ذَٰلِكَ قَدِيرًا (132) مَنْ كَانَ يُرِيدُ ثَوَابَ الدُّنْيَا فَعِنْدَ اللَّهِ
ثَوَابُ الدُّنْيَا وَالْآخِرَةِ وَكَانَ اللَّهُ سَمِيعًا بَصِيرًا (133)

127. Idan mace taji tsoron taƙadaranci daga mijinta, ko kaudakai ga buranta, to ba Laifi garesu suyi sulhu tsakaninsu. kyakkyawan sulhu a cikin rabon kwana da ciyarwa. (shine ta bar masa wani abu don fatan ya zauna tareda ita) sulhu shi yafi amfani daga rabuwa. an halicci kawuka a kan son kai, idan kuka kyautata zama da matayenku, kukaji tsoron Allah a kansu, to, Allah mai cikakken sanine da abinda kuke aiktawa

128. Bazaku sami ikon ku daidaita tsakanin mata cikin soyayya ba, ko da kun yi kwaɗayin haka, to,. kadaku ,karkata matuƙar karkata izuwa wadda kuke sonta. (a kwana da ciyarwa) ku bar "yar'uwarta kamar abar ratayewa, ita ba bazawara ba ita ba mai miji ba, idan kuka kyautata, da adalci a cikin kwana, kukaji tsoron Allah. to, haƙiƙa Ubangiji ya tabbata mai gafara ga abinda yake cikin zukatanku na daga karkatan nan, mai jinƙai.

129. Idan ma'auran suka rabu wato , ya saketa, Allah ya wadata kowanne daga cikinsu dayalwarsa, (ya bata wani mijin ya bashi wata matar,) Ubangiji ya tabbata mayalwacin falala, gwani (cikin abinda ya shirya.)

(IKON ALLAH DA WASIYYA DA TAKAWA)

130. Abinda yake cikin sammai da ƙassai yana ga Allah, haƙiƙa munyiwa waɗanda aka basu Littattafai gabanku (Yahudu da Nasara da"ya"ya yansu Amerika) daku kuma ('yan al'kur'ani) cewa kuji tsoron Allah, munce dasu daku in kun kafirce da abinda mukayi muku wasiyya dashi, to, haƙiƙa abinda yake sammai da ƙassaina Allah ne, (mallaka da halittada bauta,) Ubangiji ya tabbata mawadaci (ga buran halittada bautarsu;) abin godewa. (a cikin alherin da yake yi musu).

131. Abinda ke sammai da ƙassaina Allah ne, Allah ya isa cikakken shaida a kan haka.

132. In yaga dama saiya tafi daku Yaku mutane! yazoda waɗansu maimakonku, Ubangiji ya tabbata mai iko bisa wannan.

133. Wanda yake nufin sakamakon duniya da aikinsa, to. sakamakon duniya dana Lahira yana ga Allah shi kaɗai, kada a nemi komai sai a gunsa, Ubangiji ytabbata maiji mai gani.

(ADALCI DA SHAIDA SABODA ALLAH, DA BADA GASKIYA DA ALLAH DA LITTATTAFANSA)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُونُواْ قَوَّٰمِينَ بِٱلْقِسْطِ شُهَدَآءَ لِلَّهِ
وَلَوْ عَلَىٰٓ أَنفُسِكُمْ أَوِ ٱلْوَٰلِدَيْنِ وَٱلْأَقْرَبِينَ إِن يَكُنْ غَنِيًّا أَوْ فَقِيرًا
فَٱللَّهُ أَوْلَىٰ بِهِمَا فَلَا تَتَّبِعُواْ ٱلْهَوَىٰٓ أَن تَعْدِلُواْ وَإِن تَلْوُۥٓاْ
أَوْ تُعْرِضُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرًا ﴿134﴾ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ ءَامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَٱلْكِتَٰبِ ٱلَّذِى نَزَّلَ عَلَىٰ
رَسُولِهِۦ وَٱلْكِتَٰبِ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ مِن قَبْلُ وَمَن يَكْفُرْ بِٱللَّهِ
وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ فَقَدْ ضَلَّ ضَلَٰلًۢا بَعِيدًا ﴿135﴾
إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ثُمَّ كَفَرُواْ ثُمَّ ءَامَنُواْ ثُمَّ كَفَرُواْ ثُمَّ ٱزْدَادُواْ
كُفْرًا لَّمْ يَكُنِ ٱللَّهُ لِيَغْفِرَ لَهُمْ وَلَا لِيَهْدِيَهُمْ سَبِيلًۢا ﴿136﴾
* بَشِّرِ ٱلْمُنَٰفِقِينَ بِأَنَّ لَهُمْ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿137﴾ ٱلَّذِينَ يَتَّخِذُونَ
ٱلْكَٰفِرِينَ أَوْلِيَآءَ مِن دُونِ ٱلْمُؤْمِنِينَ أَيَبْتَغُونَ عِندَهُمُ
ٱلْعِزَّةَ فَإِنَّ ٱلْعِزَّةَ لِلَّهِ جَمِيعًا ﴿138﴾ وَقَدْ نَزَّلَ عَلَيْكُمْ فِى ٱلْكِتَٰبِ
أَنْ إِذَا سَمِعْتُمْ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ يُكْفَرُ بِهَا وَيُسْتَهْزَأُ بِهَا فَلَا تَقْعُدُواْ
مَعَهُمْ حَتَّىٰ يَخُوضُواْ فِى حَدِيثٍ غَيْرِهِۦٓ إِنَّكُمْ إِذًا مِّثْلُهُمْ
إِنَّ ٱللَّهَ جَامِعُ ٱلْمُنَٰفِقِينَ وَٱلْكَٰفِرِينَ فِى جَهَنَّمَ جَمِيعًا ﴿139﴾

ثمن

134. Ya waɗanda kuka bada gaskiya, ku kasance masu tsaiwa da adalci, masu shaida da gaskiya don Allah, koda shaiɗan nan ta kasance bisa kanku, ku faɗi gaskiya, karku ɓoye, ko bisa ma-haifanku, ko makusantanku, in abin yiwa shaidar wannan a kansa ya kasance mawadaci ko mabuƙaci, to, Allah shine mafiyi daga garesu, to, kadakubison zuciya a cikin shaidarku. in kuka jirkita shaida ko kuka bujire ga barin bada ita to, haƙiƙa Allah mai cikakken sanine da abinda kuke aikatawa.

(KARBAR ALKAWURAN SHAIHUN-NAI) WATAU SHIGA DARIKA

135. Yaku waɗanda suka bada gaskiya. ku ƙara imani da Allah da Manzonsa, da Littafin da aka saukar bisa manzonsa shine Alƙur'ani da Littattafan da aka saukar gabansa, wanda ya kafirce da Allah da Mala'ikunsa da manzanninsa, da Littattafansa, da ranar Lahira, to, haƙiƙa ya ɓata, ɓata mai nisa ga buran gaskiya.

(MUNAFUKAI DA SIFOFINSU)

136. Haƙiƙa waɗanda suka bada gaskiya da Annabi Musa (Alai hissalamu) ,sune Yahudu sannan suka kafirtada bautar ɗan maraƙi, sannan suka bada gaskiya bayan wannan, sannan suka kafirtada Annabi Isa (Alai-hissalamu), sannan suka ƙara kafirci da Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama,) Allah bazai musu gafara ba, bakuma zai shiryesu hanyar tsira ba.

137. Yiwa munafukai albishir da cewa suna da azaba mai raɗaɗi.

138. Sune waɗanda suke riƙon kafirai ababen soyayyaba muminai ba, donme suke neman izza daga garesu, to, haƙiƙa izza baki ɗayaga Allah take a duniya da Lahira, ba mai samun ta sai waliyyansa.

139. Alhali haƙiƙa ya saukar a gareku cikin Al-ƙur ani cewa idan kunji ayoyin Allah ana kafirtada ita, ana izgili da ita, wato ƙur' ani, to, kadaku ,zauna tareda kafiran nan "yan izgili.sai sun kutsa cikin wani zancen ba wannan ba, haƙiƙa ku yayin nan in kuka zauna taredasu kamar su kuke a cikin zunubi, haƙiƙa Allah mai tara munafukai da kafirai ne a cikin jahannama baki ɗaya. tamfar da suka tattara a duniya akan kafirci da izgili.

ٱلذِينَ يَتَرَبَّصُونَ بِكُمْ فَإِن كَانَ لَكُمْ فَتْحٌ مِّنَ ٱللَّهِ
قَالُوٓاْ أَلَمْ نَكُن مَّعَكُمْ وَإِن كَانَ لِلْكَٰفِرِينَ نَصِيبٌ
قَالُوٓاْ أَلَمْ نَسْتَحْوِذْ عَلَيْكُمْ وَنَمْنَعْكُم مِّنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ
فَٱللَّهُ يَحْكُمُ بَيْنَكُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ وَلَن يَجْعَلَ ٱللَّهُ لِلْكَٰفِرِينَ
عَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ سَبِيلًا ﴿140﴾ إِنَّ ٱلْمُنَٰفِقِينَ يُخَٰدِعُونَ ٱللَّهَ وَهُوَ خَٰدِعُهُمْ
وَإِذَا قَامُوٓاْ إِلَى ٱلصَّلَوٰةِ قَامُواْ كُسَالَىٰ يُرَآءُونَ ٱلنَّاسَ
وَلَا يَذْكُرُونَ ٱللَّهَ إِلَّا قَلِيلًا ﴿141﴾ مُّذَبْذَبِينَ بَيْنَ ذَٰلِكَ لَآ إِلَىٰ
هَٰٓؤُلَآءِ وَلَآ إِلَىٰ هَٰٓؤُلَآءِ وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ فَلَن تَجِدَ لَهُۥ سَبِيلًا ﴿142﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّخِذُواْ ٱلْكَٰفِرِينَ أَوْلِيَآءَ مِن دُونِ
ٱلْمُؤْمِنِينَ أَتُرِيدُونَ أَن تَجْعَلُواْ لِلَّهِ عَلَيْكُمْ سُلْطَٰنًا
مُّبِينًا ﴿143﴾ إِنَّ ٱلْمُنَٰفِقِينَ فِي ٱلدَّرْكِ ٱلْأَسْفَلِ مِنَ ٱلنَّارِ
وَلَن تَجِدَ لَهُمْ نَصِيرًا ﴿144﴾ إِلَّا ٱلذِينَ تَابُواْ وَأَصْلَحُواْ وَٱعْتَصَمُواْ
بِٱللَّهِ وَأَخْلَصُواْ دِينَهُمْ لِلَّهِ فَأُوْلَٰٓئِكَ مَعَ ٱلْمُؤْمِنِينَ وَسَوْفَ يُؤْتِ ٱللَّهُ
ٱلْمُؤْمِنِينَ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿145﴾ مَّا يَفْعَلُ ٱللَّهُ بِعَذَابِكُمْ
إِن شَكَرْتُمْ وَءَامَنتُمْ وَكَانَ ٱللَّهُ شَاكِرًا عَلِيمًا ﴿146﴾

140. Sune wađanda suke sauraran masu bin duniya a kanku idan ya kasance kuna da wani buđi daga Allah (rinjaye da ganima) sai suce daku bamu kasance bane taredaku ,(cikin addini dayaƙi bane! Ku bamu rabonmu na ganima,) idan (rabo na rinjaye) ya kasance ga kafirai sai suce dasu bamune mukayi rinjaye kanku bane, bamu ne. muka hana ku daga muminai suyi rinjaye daku ba. Sai Ubangiji yace; Allah ke hukunci tsakaninku dasu ranar al-ƙiyama, ya shigar dasu wuta ya shigar daku aljanna. Allah bazai sanya hanyar tunɓuke Musulmi ga ka-firai ba. har abada.

(SUFOFIN MUNAFUKAI HAR YAU)

141. Haƙiƙa munafukai suna bayyana yaudara ga Allah, shi ko mai kađa sune, zasu kunyata a duniya da tsinkayar da Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) a kan asirinsu da uƙuba a Lahira, idan sun tashi izuwa salla tareda muminai, saisu tashi suna masu kasala masu riyaga mutane, basa ambaton Allah sai kađan.

142. Masu dawurwura tsakanm imani da kafirci, su ba muminai basu bakafirai ba. wanda Allah ya ɓashshe shi. to, bazaka sami hanyar shiriyagareshi ba.

143. yaku wađanda suka bada gaskiya kadaku ,riƙi wađanda suka kafirta ababan .soyayyaba muminai ba, kuna sonku sanyawa Allah hujja mabayyana (a kan munafincinkune saboda jiɓintarsu.)

144. Haƙiƙa munafikai suna cikin riɓin ƙarƙas na wuta, bazaka sami mai hana musu azabar Allah ba.

145. Sai wađanda suka tubadaga munafunci, sukayi kyakkyawan aiki suka amince da Allah, suka tsarkake addininsu ga Allah daga riya, to, wađancananka suna tareda muminai, da sannu Allah zai ba muminai Lada maigirma a lahira (shine Aljanna)

146. Shin me Allah zaiyi da azabtar daku in kun gode ni'imominsa kuka bada gaskiya dashi. Ubangiji ya tabbata mai godiyaga aikin muminai, masani da halitta.

(BAYYANAWA DA MUMMUNAR MAGANA DA HATSARINTA)

حزب

۞ لَّا يُحِبُّ اُ۬للَّهُ اُ۬لْجَهْرَ بِالسُّوٓءِ مِنَ اَ۬لْقَوْلِ إِلَّا مَن ظُلِمَ وَكَانَ اَ۬للَّهُ
سَمِيعاً عَلِيماً ﴿147﴾ إِن تُبْدُواْ خَيْراً اَوْ تُخْفُوهُ أَوْ تَعْفُواْ عَن سُوٓءٖ
فَإِنَّ اَ۬للَّهَ كَانَ عَفُوّاً قَدِيراً ﴿148﴾ إِنَّ اَ۬لذِينَ يَكْفُرُونَ بِاللَّهِ
وَرُسُلِهِۦ وَيُرِيدُونَ أَن يُّفَرِّقُواْ بَيْنَ اَ۬للَّهِ وَرُسُلِهِۦ وَيَقُولُونَ
نُؤْمِنُ بِبَعْضٖ وَنَكْفُرُ بِبَعْضٖ وَيُرِيدُونَ أَن يَّتَّخِذُواْ بَيْنَ ذَٰلِكَ
سَبِيلاً ﴿149﴾ اُوْلَٰٓئِكَ هُمُ اُ۬لْكَٰفِرُونَ حَقّاً وَأَعْتَدْنَا لِلْكَٰفِرِينَ
عَذَاباً مُّهِيناً ﴿150﴾ وَالذِينَ ءَامَنُواْ بِاللَّهِ وَرُسُلِهِۦ وَلَمْ يُفَرِّقُواْ
بَيْنَ أَحَدٖ مِّنْهُمُۥٓ أُوْلَٰٓئِكَ سَوْفَ نُؤْتِيهِمُۥٓ أُجُورَهُمْ وَكَانَ اَ۬للَّهُ
غَفُوراً رَّحِيماً ﴿151﴾ يَسْـَٔلُكَ أَهْلُ اُ۬لْكِتَٰبِ أَن تُنَزِّلَ عَلَيْهِمْ كِتَٰباً
مِّنَ اَ۬لسَّمَآءِ فَقَدْ سَأَلُواْ مُوس۪يٰٓ أَكْبَرَ مِن ذَٰلِكَ فَقَالُوٓاْ أَرِنَا اَ۬للَّهَ
جَهْرَةً فَأَخَذَتْهُمُ اُ۬لصَّٰعِقَةُ بِظُلْمِهِمْ ثُمَّ اَ۪تَّخَذُواْ اُ۬لْعِجْلَ
مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَتْهُمُ اُ۬لْبَيِّنَٰتُ فَعَفَوْنَا عَن ذَٰلِكَ وَءَاتَيْنَا
مُوس۪يٰ سُلْطَٰناً مُّبِيناً ﴿152﴾ وَرَفَعْنَا فَوْقَهُمُ اُ۬لطُّورَ
بِمِيثَٰقِهِمْ وَقُلْنَا لَهُمُ اُ۟دْخُلُواْ اُ۬لْبَابَ سُجَّداً وَقُلْنَا لَهُمْ
لَا تَعْدُواْ فِي اِ۬لسَّبْتِ وَأَخَذْنَا مِنْهُم مِّيثَٰقاً غَلِيظاً ﴿153﴾

147. Allah bayason bayyanawa da mummunar magana sai wanda aka zalunce shi, (to, wannan yana iya kai ƙara, ko kuma yayi mugunyar addu'a,) Ubangiji ya tabbata mai ji, masani.

148. In kun bayyana alheri. ko kuka ɓoyeshi ko kukayi rangwame (ga wanda ya zalunce ku,) to, haƙiƙa Allah ya tabbata mai rangwame mai iko.

(KAFIRCI DA IMANI DA ƘARSHEN KOWANNE)

149. Haƙiƙa waɗanda suka kafirtada Allah da manzanninsa, suke nufin su rarrabe tsakanin Allah da manzanninsa, su bada gaskiya dashi ba taredasu ba, suke cewa; "Mun bada gaskiya da sashin manzanni mun kafirce da sashi suke nufin su riƙi hanya tsakanin waɗancananka.

150. waɗancanenka sune kafirai na gaske, mun tanadi azaba mai wulaƙantarwa ga kafirai.

151. Waɗanda suka bada gaskiya da Allah da manzanninsa basu rarrabe tsakanin daya daga garesu ba, to waɗannan da sannu dai zamu basu Ladansu, Ubangiji ya tabbata mai gafara mai jinƙai.

(WANI ABU DAGA MIYAGUN AYYUK.AN YAHUDAWA)

152. Ahalul-Kitabi (Yahudu) suna tambayar ka, ka saukar da Littafi garesu daga sama (gabadaya,) tamkar da aka saukar bisa Annabi Musa (Alai-hissalamu, don ta'annati,) haƙiƙa iyayensu sun tambayi Annabi Musa (Alai-hissalamu) mafi girma daga haka, sukace "Nuna mana Allah ƙarara", tsawa ta kamasu, saboda zaluncinsu. (wato tsawar mutuwa ta hallakar dasu. saboda tambayon ta'annuti,) sannan suka riƙi ɗan maraƙi ubangiji garesu, bayan hujjoji mabayyana sunzo musu. (masu nuna kaɗaitar Allah) mukayi rangwame ga wancananka (bamu tunɓike su ba,) muka baiwa Annabi Musa (Alai-hissalamu) hujja mabayyaniya (shine umarninsu da kisan kansu wajen tubasuka kwayi).

153. Kuma muka ɗaga dutse birbishinsu saboda riƙon al-ƙawarinsu, mukace dasu (alhali shi dutsen nan yayi musu inuwa bisansu,) "Ku shiga ƙofar garin kuna masu sujjada, mukace dasu "Kada kuyi shisshigi a cikin su ranar Asabar, "mun riƙi al-ƙawari kakkaura a kansu a kan wannan, (suka warware).

فَبِمَا نَقْضِهِم مِّيثَٰقَهُمْ وَكُفْرِهِم بِـَٔايَٰتِ اِ۬للَّهِ وَقَتْلِهِمُ اُ۬لْأَنۢبِيٓـَٔاءَ
بِغَيْرِ حَقٍّ وَقَوْلِهِمْ قُلُوبُنَا غُلْفٌۢ بَلْ طَبَعَ اَ۬للَّهُ عَلَيْهَا بِكُفْرِهِمْ
فَلَا يُؤْمِنُونَ إِلَّا قَلِيلًا ﴿154﴾ وَبِكُفْرِهِمْ وَقَوْلِهِمْ عَلَىٰ مَرْيَمَ بُهْتَٰنًا
عَظِيمًا ﴿155﴾ وَقَوْلِهِمْ إِنَّا قَتَلْنَا اَ۬لْمَسِيحَ عِيسَى اَ۪بْنَ مَرْيَمَ رَسُولَ اَ۬للَّهِ
وَمَا قَتَلُوهُ وَمَا صَلَبُوهُ وَلَٰكِن شُبِّهَ لَهُمْ وَإِنَّ اَ۬لَّذِينَ
اَ۪خْتَلَفُواْ فِيهِ لَفِي شَكٍّ مِّنْهُ مَا لَهُم بِهِۦ مِنْ عِلْمٍ إِلَّا اَ۪تِّبَاعَ اَ۬لظَّنِّ
وَمَا قَتَلُوهُ يَقِينَۢا ﴿156﴾ بَل رَّفَعَهُ اُ۬للَّهُ إِلَيْهِ وَكَانَ اَ۬للَّهُ
عَزِيزًا حَكِيمًا ﴿157﴾ * وَإِن مِّنْ أَهْلِ اِ۬لْكِتَٰبِ إِلَّا لَيُؤْمِنَنَّ بِهِۦ ثمن
قَبْلَ مَوْتِهِۦ وَيَوْمَ اَ۬لْقِيَٰمَةِ يَكُونُ عَلَيْهِمْ شَهِيدًا ﴿158﴾ فَبِظُلْمٍ مِّنَ
اَ۬لَّذِينَ هَادُواْ حَرَّمْنَا عَلَيْهِمْ طَيِّبَٰتٍ أُحِلَّتْ لَهُمْ وَبِصَدِّهِمْ عَن
سَبِيلِ اِ۬للَّهِ كَثِيرًا ﴿159﴾ وَأَخْذِهِمُ اُ۬لرِّبَوٰاْ وَقَدْ نُهُواْ عَنْهُ وَأَكْلِهِمْ أَمْوَٰلَ
اَ۬لنَّاسِ بِالْبَٰطِلِ وَأَعْتَدْنَا لِلْكَٰفِرِينَ مِنْهُمْ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿160﴾
لَّٰكِنِ اِ۬لرَّٰسِخُونَ فِي اِ۬لْعِلْمِ مِنْهُمْ وَالْمُؤْمِنُونَ يُؤْمِنُونَ بِمَا أُنزِلَ إِلَيْكَ
وَمَا أُنزِلَ مِن قَبْلِكَ وَالْمُقِيمِينَ اَ۬لصَّلَوٰةَ وَالْمُؤْتُونَ اَ۬لزَّكَوٰةَ
وَالْمُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ وَالْيَوْمِ اِ۬لْأٓخِرِ أُوْلَٰٓئِكَ سَنُؤْتِيهِمْ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿161﴾

154. To, saboda warware al-ƙawarinsune da kafircewarsu da ayoyin Allah, da kashewarsu Annabawa bada gaskiya ba, da faɗinsu ga Ma'aikin Allah (Sallallahu alaihi wasallama) "Zukatanmu rufaffu ne, "muka tsine musu albarka, haba! Allah ya yimke a kanta ne saboda kafircinsu, to, bazasu bada gaskiyaba sai kaɗan daga cikinsu (kamar Abdullahi Ibn Salami da abokansa).

155. Kuma da kafircinsu (a marra ta biyu da Annabi Isa (Alai-hissalamu) da girba ƙarya da sukayi mai girma a bisa Nana Maryamu (yardar Allah ta tabbata a gareta yadda suka jefe tada zina).

156. Da faɗinsu (suna masu fariya,) haƙiƙa mune muka kashe Al-masihu Isa Dan Maryama jakadan Allah (a cikin riyawarsu Ubangiji ya ƙaryata su da faɗinsa,) basu kashe shiba basu tsire shiba, saidai an kamanta abin kashewan nan da tsirewar nan garesu ne, (suka zaci Annabi Isa ne 'Alai-hissalamu') haƙiƙa waɗanda sukayi tanbaba a cikin Annabi Isa Alai-hissalamu Lallai suna cikin kokwanto daga gareshi, (sashinsu yana faɗa; fuskar dai fuskar Annabi Isa ce, amma jikin ba nasa bane, waɗansu sukace kai shine,) basu da wani abu na sani a cikin kashe shi, sai bin zato kawai, basu kashe shi suna masu sakankancewa ba.

157. Bari' Aah ya dauke shine izuwa gareshi, Ubangiji ya tabbata mabuwayi (cikin mulkinsa) gwani (cikin aikinsa).

158. Babu ɗaya daga mazowa Littafi face zai bada gaskiya da Annabi Isa (Alai-haissalamu) gaban mutuwar Annabi Isan, (sabodazai sauka gabada tashin Al-ƙiyama kamar yadda Hadisi yazoda haka) ranar Al-ƙiyama Annabi Isa (Alai-hissalamu) zai kasance shaiɗa a kansu (a kan abinda suka aikata).

(WANI ABU NA DAGA MIYAGUN AYYUKAN YAHUDU DA SAKAMAKONSU)

159. Saboda zalunci daga Yahudu muka haramta musu daga daɗaɗa da aka halatta musu, da kuma hanawar su mutane ga buran addinin Allah; hanawa mai yawa.

160. Da karɓar riba alhali an hana su ga buranta (a cikin Attaura,) da cin dukiyoyin mutane, da ƙarya, Mun tanadi azaba mai' raɗaɗi ga kafirai daga cikinsu.

161. Sai dai masu tabbataccen sani daga cikinsu da mummai (muhajirai ke nan da Ansaru) sun bada gaskiya da abinda aka saukar izuwa gareka, da abinda aka saukar gabanka (na daga Littattafai,) da masu tsaida salla daidai wadaida, da masu bada zakka da waɗanda suka bada gaskiya da Allah da ranar Lahira, waɗancananka da sannu zamu basu Lada mai girma.

إِنَّا أَوْحَيْنَا إِلَيْكَ كَمَا أَوْحَيْنَا إِلَىٰ نُوحٍ وَالنَّبِيِّينَ مِنْ
بَعْدِهِ وَأَوْحَيْنَا إِلَىٰ إِبْرَاهِيمَ وَإِسْمَاعِيلَ وَإِسْحَاقَ وَيَعْقُوبَ
وَالْأَسْبَاطِ وَعِيسَىٰ وَأَيُّوبَ وَيُونُسَ وَهَارُونَ وَسُلَيْمَانَ
وَآتَيْنَا دَاوُودَ زَبُورًا ﴿162﴾ وَرُسُلًا قَدْ قَصَصْنَاهُمْ عَلَيْكَ
مِنْ قَبْلُ وَرُسُلًا لَمْ نَقْصُصْهُمْ عَلَيْكَ وَكَلَّمَ اللَّهُ
مُوسَىٰ تَكْلِيمًا ﴿163﴾ رُسُلًا مُبَشِّرِينَ وَمُنْذِرِينَ لِئَلَّا يَكُونَ
لِلنَّاسِ عَلَى اللَّهِ حُجَّةٌ بَعْدَ الرُّسُلِ وَكَانَ اللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمًا ﴿164﴾
لَٰكِنِ اللَّهُ يَشْهَدُ بِمَا أَنْزَلَ إِلَيْكَ أَنْزَلَهُ بِعِلْمِهِ وَالْمَلَائِكَةُ
يَشْهَدُونَ وَكَفَىٰ بِاللَّهِ شَهِيدًا ﴿165﴾ إِنَّ الَّذِينَ كَفَرُوا وَصَدُّوا عَنْ
سَبِيلِ اللَّهِ قَدْ ضَلُّوا ضَلَالًا بَعِيدًا ﴿166﴾ إِنَّ الَّذِينَ كَفَرُوا وَظَلَمُوا
لَمْ يَكُنِ اللَّهُ لِيَغْفِرَ لَهُمْ وَلَا لِيَهْدِيَهُمْ طَرِيقًا ﴿167﴾
إِلَّا طَرِيقَ جَهَنَّمَ خَالِدِينَ فِيهَا أَبَدًا وَكَانَ ذَٰلِكَ عَلَى اللَّهِ
يَسِيرًا ﴿168﴾ يَا أَيُّهَا النَّاسُ قَدْ جَاءَكُمُ الرَّسُولُ بِالْحَقِّ
مِنْ رَبِّكُمْ فَآمِنُوا خَيْرًا لَكُمْ وَإِنْ تَكْفُرُوا فَإِنَّ لِلَّهِ
مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ وَكَانَ اللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمًا ﴿169﴾

ربع

(KADAITAR WAHAYI DA HIKIMAR AIKO MANZANNI ALAIHIMU-S-SALAMU

162. Hakika mu, mun aiko izuwa gareka tamfar da muka aiko izuwa Annabi Nuhu (Alai-hissalamu) da Annabawa daga bayansa, tamfar da muka aiko izuwa Annabi Ibrahim da Isma'ila da Ishaka, ("ya"yansa,) dayakubu (đan Ishaka,) da "ya"yan Annabi yakubada Annabi Isa, da Ayuba, da Yunusa da Haruna dasulaiman (Alai-hissalamu) mun baiwa Annabi Dawuda (Alai-hissalamu) Zabura.

163. Mun aiko manzanni da muka Labarta su a gareka, da wanđanda bamu Labarta maka ba. Allah ya zantar da Annabi Musa (Alai-hissalamu) bada tsakaniba, zantarwa.

164. Jakadu masu albishir da masu tsoratarwa, don kada mutane su zama suna da hujja akan Ubangiji, Ubangiji ya tabbata mabuwayi mai hikima.

165. Sai dai Allah yana shaidarwa da abinda ya saukar izuwa gareka, ya saukar dashine da ilminsa, Mala'ikunsa sun shaidar Allah ya isa shaida.

(SAKAMAKON KAFIRCI)

166. Hakika wađanda suka kafirta suka tsare mutane shiga addinin Allah, hakika sun ɓata, ɓata mai nisa ga buran gaskiya).

167. Hakika wađanda suka kafirta suka zalinci (Annabi "Sallallahu alaihi wasallama') Allah bazaiyi musu gafara ba, bazai shiryesu hanyar tsira ba,

168. Sai hanyar jahannama, masu dawwama cikinta har abada, wancananka ya tabbata mai sauki ga Allah.

169. Yaku wađannan mutane, hakika manzo (Sallallahu alaihi wasallama) yazo mukuda gaskiya daga Ubangijinku, ku bada gaskiya, ku nufi alheri gareku, idan kun kafirta, to, hakika mulkin sammai da kassaina ga Allah, Ubangiji ya tabbata mai sani mai hikima.

(HAKIKAR ANNABI ISA 'ALAI-HISSALAMU' A CIKIN ALKUR' ANI)

يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ لَا تَغْلُواْ فِي دِينِكُمْ وَلَا تَقُولُواْ عَلَى ٱللَّهِ
إِلَّا ٱلْحَقَّۚ إِنَّمَا ٱلْمَسِيحُ عِيسَى ٱبْنُ مَرْيَمَ رَسُولُ ٱللَّهِ
وَكَلِمَتُهُۥٓ أَلْقَىٰهَآ إِلَىٰ مَرْيَمَ وَرُوحٌ مِّنْهُۖ فَـَٔامِنُواْ
بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦۖ وَلَا تَقُولُواْ ثَلَٰثَةٌۚ ٱنتَهُواْ خَيْرًا لَّكُمْۚ
إِنَّمَا ٱللَّهُ إِلَٰهٌ وَٰحِدٌۖ سُبْحَٰنَهُۥٓ أَن يَكُونَ لَهُۥ وَلَدٌۘ لَّهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَمَا فِي ٱلْأَرْضِۗ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلًا ﴿170﴾ * لَّن يَسْتَنكِفَ ٱلْمَسِيحُ ثمن
أَن يَكُونَ عَبْدًا لِّلَّهِ وَلَا ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ ٱلْمُقَرَّبُونَۚ وَمَن
يَسْتَنكِفْ عَنْ عِبَادَتِهِۦ وَيَسْتَكْبِرْ فَسَيَحْشُرُهُمْ إِلَيْهِ جَمِيعًا ﴿171﴾
فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَيُوَفِّيهِمْ أُجُورَهُمْ
وَيَزِيدُهُم مِّن فَضْلِهِۦۖ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ ٱسْتَنكَفُواْ وَٱسْتَكْبَرُواْ
فَيُعَذِّبُهُمْ عَذَابًا أَلِيمًا وَلَا يَجِدُونَ لَهُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ
وَلِيًّا وَلَا نَصِيرًا ﴿172﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ قَدْ جَآءَكُم
بُرْهَٰنٌ مِّن رَّبِّكُمْ وَأَنزَلْنَآ إِلَيْكُمْ نُورًا مُّبِينًا ﴿173﴾
فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَٱعْتَصَمُواْ بِهِۦ فَسَيُدْخِلُهُمْ فِي رَحْمَةٍ
مِّنْهُ وَفَضْلٍ وَيَهْدِيهِمْ إِلَيْهِ صِرَٰطًا مُّسْتَقِيمًا ﴿174﴾

170. Yaku mazowa Littafi kada kuyi shishshigi a cikin addinmku, kuma kadaku ,faɗi (komai) gameda Zatin Ubangiji; sai gaskiya, Shi Annabi Isa 'Alai-hissalamu' jakadan Allah ne shi, kalma tasa ce ya sadata izuwa Nana Maryamu, ma' abocin rai ne daga Allah, to, ku bada gakiya da Allah da manzanninsa, kada kuce iyayen giji uku ne, (Allah da Isa da uwarsa) ku hanu (ga buran wannan) shi yafi a gareku, haƙiƙa Allah dai Ubangiji ne makaɗaicin sarki, tsarki ya tabbata gareshi ga buran ya zama yana da ɗa, abinda yake sammai da ƙassai duk nasane, Allah ya tabbata masani da haka.

171. Annabi Isa (Alai-hissalamu) baya ƙyamar ya kasance bawa ga Allah, wala Mala'iku ababan kusantawa, duka wanda yayi ƙyama ga buran bautar Allah, yayi girman kai, da sannu Allah zai tarasu izuwa gareshi baki ɗaya.

172. Amma waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagari, to, yana cika musu Ladansu, yana ƙara musu daga cikin falalarsa (abinda ido bai ganibakunne bai ji ba zuciya bata ɗarsa ba,) amma waɗanda sukayi ƙyama sukayi girman kai, to, zaiyi musu azaba, azaba mai raɗaɗi, bazasu sami majiɓinci ba Allah ba wala mai taimako.

(KIRA IZUWA ALLAH)

173. Yaku waɗannan mutane. haƙiƙa hujja tazo muku daga Ubangijinku (shine Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) mun saukar da haske mabayyani izuwa gareku (shine Al-ƙur'ani).

174. To, amma waɗanda suka bada gaskiya da Allah, suka ƙanƙame wa Allah, da sannu zai shigar dasu a cikin rahama daga gareshi da falala, ya shiryesu hanya madaidaiciya izuwa gareshi (Addinin Musulunci).

(HAƘƘIN 'YAN'UWA MAZA A CIKIN GADO)

يَسْتَفْتُونَكَ قُلِ ٱللَّهُ يُفْتِيكُمْ فِي ٱلْكَلَٰلَةِ إِنِ ٱمْرُؤٌا۟ هَلَكَ
لَيْسَ لَهُۥ وَلَدٌ وَلَهُۥٓ أُخْتٌ فَلَهَا نِصْفُ مَا تَرَكَ وَهُوَ يَرِثُهَآ
إِن لَّمْ يَكُن لَّهَا وَلَدٌ فَإِن كَانَتَا ٱثْنَتَيْنِ فَلَهُمَا ٱلثُّلُثَانِ مِمَّا تَرَكَ
وَإِن كَانُوٓا۟ إِخْوَةً رِّجَالًا وَنِسَآءً فَلِلذَّكَرِ مِثْلُ حَظِّ
ٱلْأُنثَيَيْنِ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمْ أَن تَضِلُّوا۟ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمٌۢ ﴿175﴾

5 سُورَةُ المَائِدَةِ مَدَنِيَّةٌ

وَهِيَ مِائَةٌ وَثِنْتَانِ وَعِشْرُونَ ءَايَةً 122

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَوْفُوا۟ بِٱلْعُقُودِ ﴿1﴾ أُحِلَّتْ لَكُم بَهِيمَةُ ٱلْأَنْعَٰمِ
إِلَّا مَا يُتْلَىٰ عَلَيْكُمْ غَيْرَ مُحِلِّى ٱلصَّيْدِ وَأَنتُمْ حُرُمٌ إِنَّ ٱللَّهَ يَحْكُمُ مَا يُرِيدُ ﴿2﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تُحِلُّوا۟ شَعَٰٓئِرَ ٱللَّهِ وَلَا ٱلشَّهْرَ ٱلْحَرَامَ
وَلَا ٱلْهَدْىَ وَلَا ٱلْقَلَٰٓئِدَ وَلَآ ءَآمِّينَ ٱلْبَيْتَ ٱلْحَرَامَ يَبْتَغُونَ فَضْلًا
مِّن رَّبِّهِمْ وَرِضْوَٰنًا وَإِذَا حَلَلْتُمْ فَٱصْطَادُوا۟ وَلَا يَجْرِمَنَّكُمْ شَنَـَٔانُ قَوْمٍ
أَن صَدُّوكُمْ عَنِ ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ أَن تَعْتَدُوا۟ وَتَعَاوَنُوا۟ عَلَى ٱلْبِرِّ وَٱلتَّقْوَىٰ
وَلَا تَعَاوَنُوا۟ عَلَى ٱلْإِثْمِ وَٱلْعُدْوَٰنِ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ إِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ﴿3﴾

175. Suna neman fatawarka a cikin bakarara, Cene Allah yanayi muku jawabi a cikin bakarara, in mutum ya mutu bashi da ɗa, bashi da uba, (bakarara ke nan) alhali yana da "yar"uwa shaƙiƙiyako ta wajen uwa ko uba, to, tana da rabin abinda ya bari, shi dan' uwan nan nata shine zai gaji dukkan abindata bari in batada ɗa, in kuwa "yan" uwa mata suka zama biyu da abinda yafi haka, to, suna dasulusani daga abinda ɗan'uwan ya bari, in kuwa "yan' uwan sun kasance mazaje da mataye, to, namiji yana da misalin . rabon mace biyu, Allah yanayi muku bayanin (shari' o' in addininsa) don kadaku ,ɓata, Allah masanine da komai

Suratul Ma'idati

A Madina Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Dari Da Ishirin Da Biyu (122)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe

(CIKA ALƘAWURA YANA DAGA CIKIN AL-ƘAWARIN SHAIHUNAN GASKIYA)

1. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya, ku cika al-ƙawura (wacce take tsakaninkuda Allah da kuma mutane).

(HALACCIN DABBOBI)

2. An Halatta muku dabban nan ta busashe (raƙumi, shanu, tumaki, aci bayan an yanka,) sai abinda ake karanta (haramcinsa) a gareku, ba masu halatta farauta alhali kunaɗaure da harami ba.Korewar bukata a cikin aikace-aikacen Allah da kuma hukunce-hukuncensa) "Allah Ubangiji yana hukunta abinda ya nufa".

(HARAMCIN FARAUTA A CIKIN IHRAMI)

3. Yaku waɗanda suka bada gaskiya kadaku ,halatta alamomin addinin Allah (da farauta a cikin Ihrami,) kadaku ,halatta wata mai alfarma (dayaƙi a cikinsa,) kadaku ,halatta hadaya (da bujira gareta,) kadaku ,halatta ratayé-rataye da aka rataya wa hadaya, kadaku ,halatta manufata ga Dakin Allah mai alfarma, (wato kadaku ,yaƙe su) waɗanda kuke neman arziki daga Ubangijinsu ta wajen ciniki,) suke neman yaddar Allah, to, idan kun warware haramin Kuyi farauta, Kada ġabata mutane Don sun , hana 'ku masallaci mai alfarma tasa Kuyi shisshigi a Ƙansu da Kisa Ko Waninsa

(WAJABCIN TAIMAKON JUNA A KAN SHA'ANIN ALHERI)

"Ku taimaki juna a kan sha' anin alheri da tsoron Allah, kadaku ,taimaki juna a kan saɓon Allah dashisshigi (a cikin haddodin Allah,) kuji tsoron Allah, haƙiƙa Allah mai tsananin azabane (ga wanda ya saɓe shi)".

(HARAMCIN MUSHE DA WANINSA)

ربع

* حُرِّمَتْ عَلَيْكُمُ الْمَيْتَةُ وَالدَّمُ وَلَحْمُ الْخِنزِيرِ وَمَا أُهِلَّ
لِغَيْرِ اللَّهِ بِهِ وَالْمُنْخَنِقَةُ وَالْمَوْقُوذَةُ وَالْمُتَرَدِّيَةُ وَالنَّطِيحَةُ وَمَا
أَكَلَ السَّبُعُ إِلَّا مَا ذَكَّيْتُمْ وَمَا ذُبِحَ عَلَى النُّصُبِ وَأَن تَسْتَقْسِمُوا
بِالْأَزْلَامِ ذَٰلِكُمْ فِسْقٌ الْيَوْمَ يَئِسَ الَّذِينَ كَفَرُوا مِن دِينِكُمْ
فَلَا تَخْشَوْهُمْ وَاخْشَوْنِ الْيَوْمَ أَكْمَلْتُ لَكُمْ دِينَكُمْ وَأَتْمَمْتُ
عَلَيْكُمْ نِعْمَتِي وَرَضِيتُ لَكُمُ الْإِسْلَامَ دِينًا فَمَنِ اضْطُرَّ
فِي مَخْمَصَةٍ غَيْرَ مُتَجَانِفٍ لِّإِثْمٍ فَإِنَّ اللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿4﴾
يَسْأَلُونَكَ مَاذَا أُحِلَّ لَهُمْ قُلْ أُحِلَّ لَكُمُ الطَّيِّبَاتُ وَمَا عَلَّمْتُم
مِّنَ الْجَوَارِحِ مُكَلِّبِينَ تُعَلِّمُونَهُنَّ مِمَّا عَلَّمَكُمُ اللَّهُ فَكُلُوا
مِمَّا أَمْسَكْنَ عَلَيْكُمْ وَاذْكُرُوا اسْمَ اللَّهِ عَلَيْهِ وَاتَّقُوا اللَّهَ
إِنَّ اللَّهَ سَرِيعُ الْحِسَابِ ﴿5﴾ الْيَوْمَ أُحِلَّ لَكُمُ الطَّيِّبَاتُ وَطَعَامُ
الَّذِينَ أُوتُوا الْكِتَابَ حِلٌّ لَّكُمْ وَطَعَامُكُمْ حِلٌّ لَّهُمْ وَالْمُحْصَنَاتُ مِنَ
الْمُؤْمِنَاتِ وَالْمُحْصَنَاتُ مِنَ الَّذِينَ أُوتُوا الْكِتَابَ مِن قَبْلِكُمْ إِذَا
آتَيْتُمُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ مُحْصِنِينَ غَيْرَ مُسَافِحِينَ وَلَا مُتَّخِذِي أَخْدَانٍ
وَمَن يَكْفُرْ بِالْإِيمَانِ فَقَدْ حَبِطَ عَمَلُهُ وَهُوَ فِي الْآخِرَةِ مِنَ الْخَاسِرِينَ ﴿6﴾

4. An haramta muku cin mushe da jini abin zubarwa, da naman alhanzir, da abinda aka ambaci wanin Allah a yankansa, da dabbar da aka shaƙe, da wacce aka raɗe, da wacce ta faɗo daga sama, da sokakkiya da ƙaho, da abinda namun jeji sukaci, sai abinda kuka riski yankansa (bada an zartar da makasarsa ba) da abinda aka yanka a kan sunan gumaka, an haramta muku kuyi rabo ko kuyi. hukunci da ƙyamare, (a zamanin jahiliyya suke wannan aiki, sukan ajiyeta a wajen mai tsaron Ka' abasu sarautata, yayin fitowar alamar umarni ko alamar hani, wato If-al ko Lataf-al, kuri'a tana daga ciki) Wancananka fasiƙanci ne.

(ƘARFIN MUSULUNCI A RANAR ARFA A SHEKARAR HAJJIN BAN KWANA, ALLAH YA SAUKAR DA:)

A yau waɗanda suka kafirta sun ɗebe ƙauna daga riddarku ga buran addininku, to, kada kuji tsoronsu, kuji tsorona, a yau na cika muku addininku, na cika ni'imata a gareku, na yarda da Musulunci addini a garekuda wanda aka buƙatar dashi (a cikin yunwa izuwa cin wani abu daga abinda aka haramta a gareshi yaci) ba mai karkata izuwa saɓo ba, to, haƙiƙa Ubangiji mai gafara ne a gareshi mai jinƙai (a cikin halatta masa shi).

(HALAL DAGA ABINCI DA WANINSA)

5. Suna tambayarka ya Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) Me aka halatta garesu (na daga abinci?) Cene "an halatta muku daɗaɗa da farautar abinda kuka koyawa farauta na daga masuyin miki, (karnuka da tsuntsaye da waninsu,) kuna masu cunasu masu koya musu sanin yadda zasu kama farauta daga abinda Allah yasanar daku, (na daga Ladaban farauta,) to, kuci daga abinda suka kama a gareku, ku ambaci sunan Ubangiji a kansa (yayin sakinsa). Kuji tsoron Allah, Ubanglji mai gaggawar sakamako ne.
6. A yau an halalta muku daɗaɗa da abincin waɗanda aka basu Littafi (wato yanke-yanken Yahudu da Nasara) halal ne gareku, abincin ku halal ne a garesu, da katangantattu na daga mumlnai mataye, daga katangantattu na "ya'yayen waɗanda aka basu Littafi gabanku, idan kun basu sadakansu kuna masu aure dasu ba masu bayyana zina dasu ba, bakuna masu riƙon abokai daga cikinsu (kuna zina dasu a ɓoye ba. Wanda yayi ridda haƙiƙa aikinsa ya watse, Allah ya kiyashe mu Amin) shi a Lahira yana daga cikin taɓaɓɓu, (in ya mutu murtaddi).

(ALWALA DA WANKA DA TAIMANA)

ثمن

* يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا قُمْتُمُۥٓ إِلَى ٱلصَّلَوٰةِ فَٱغْسِلُواْ
وُجُوهَكُمْ وَأَيْدِيَكُمُۥٓ إِلَى ٱلْمَرَافِقِ وَٱمْسَحُواْ بِرُءُوسِكُمْ
وَأَرْجُلَكُمْ إِلَى ٱلْكَعْبَيْنِ وَإِن كُنتُمْ جُنُباً فَٱطَّهَّرُواْ
وَإِن كُنتُم مَّرْضَىٰٓ أَوْ عَلَىٰ سَفَرٍ اَوْ جَآءَ أَحَدٌ مِّنكُم
مِّنَ ٱلْغَآئِطِ أَوْ لَمَسْتُمُ ٱلنِّسَآءَ فَلَمْ تَجِدُواْ مَآءً فَتَيَمَّمُواْ
صَعِيداً طَيِّباً فَامْسَحُواْ بِوُجُوهِكُمْ وَأَيْدِيكُم مِّنْهُ
مَا يُرِيدُ ٱللَّهُ لِيَجْعَلَ عَلَيْكُم مِّنْ حَرَجٍ وَلَٰكِن يُرِيدُ
لِيُطَهِّرَكُمْ وَلِيُتِمَّ نِعْمَتَهُۥ عَلَيْكُمْ لَعَلَّكُمْ
تَشْكُرُونَ ۝7 وَاذْكُرُواْ نِعْمَةَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ
وَمِيثَٰقَهُ ٱلَّذِے وَاثَقَكُم بِهِۦٓ إِذْ قُلْتُمْ سَمِعْنَا وَأَطَعْنَا
وَاتَّقُواْ ٱللَّهَ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ۝8 يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
كُونُواْ قَوَّٰمِينَ لِلَّهِ شُهَدَآءَ بِالْقِسْطِ وَلَا يَجْرِمَنَّكُمْ شَنَـَٔانُ قَوْمٍ
عَلَىٰٓ أَلَّا تَعْدِلُواْ اُعْدِلُواْ هُوَ أَقْرَبُ لِلتَّقْوَىٰ وَاتَّقُواْ ٱللَّهَ
إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرٌۢ بِمَا تَعْمَلُونَ ۝9 وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُم مَّغْفِرَةٌ وَأَجْرٌ عَظِيمٌ ۝10

7. Yaku waɗanda suka bada gaskiya, idan kun nufin tashi izuwa salla, (alhali kuna masu kari,) to, ku wanke fuskokin kuda hannayen ku izuwa gwuiwoyin hannu, (wato tareda gwuiwoyin,) kuyi shafa ga kawunanku, ku wanke kafafuwanku, izuwa idondunan sawu guda biyu, idan kun kasance masu janaba, to, kuyi wanka, idan kun kasance marasa Lafiya, (rashin Lafiyar da ruwa zai cutar,) ko, bisa tafiya, ko ɗayanku yazo daga makewayi (wato yayi kari.) ko kuka tarada mata, baku sami ruwa ba (bayan nemansa,) to, saiku nufi turɓaya tsarkakka sai kuyi shafa da fuskokinkuda hannayenku daga turɓayar nan, Allah baya nufin yasanya ƙunci a gareku, saboda haka ya wajabta muku taimana , maimakon alwalla da wanka. Kai dai yana nufin ya tsarkake kune daga karuruwa da zunubai, kuma donya cika ni'ima tasa (da Musulunci a garekuda bayanin shari'o'in addinin) don ku gode wa (ni'imominsa).
8. Ku ambaci ni'imar Allah a gareku (da Musulunci) da al-ƙawarinsa. wanda yayi muku al-ƙawari a kansa zamanin da kuka faɗa (ga Manzon Allah, tsiran Allah da amincinsa ya tabbata a gareshi, yayin da kukayi mabaya'a dashi,) "Munji munbi (a cikin dukkan abinda kake umarninmu dashi ko kake haninmu daga abinda muke so ko Barna so)". Kuji tsoron Allah (a cikin al-ƙawarinsa kadaku ,warware,) haƙiƙa Ubangiji Masanine da haluluwan ƙiraza.

(INGANTA AIKI DA SHAIDA DA ADALCI DA GODE NI'IMOMIN ALLAH)

9. Yaku waɗanda suka bada gaskiya, ku kasanse masu matuƙar tsayawa da haƙƙokin Allah masu shaidawa da adalci, kada gabar mutane ta dauƙe ku, a kan kada kuyi adalci, kuyi adalci (a cikin masoyi da maƙiyi,) shi adalci shine mafi kusanci izuwa tsoron Allah. Kuji tsoron Allah, haƙiƙa Ubangiji mai cikakken sanine da abinda kuke aikatawa.
10. Allah ya al-ƙawarta waɗanda suka bada gaskiya, sukayi ayyuka nagari al-ƙawari kyakkyawa, gafara ta tabbata garesu da Lada mai girma (aljanna).

وَالَّذِينَ كَفَرُوا وَكَذَّبُوا بِـَٔايَٰتِنَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ الْجَحِيمِ ﴿11﴾
يَٰٓأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُوا اذْكُرُوا نِعْمَتَ اللَّهِ عَلَيْكُمْ
إِذْ هَمَّ قَوْمٌ أَن يَبْسُطُوٓا إِلَيْكُمْ أَيْدِيَهُمْ فَكَفَّ
أَيْدِيَهُمْ عَنكُمْ وَاتَّقُوا اللَّهَ وَعَلَى اللَّهِ فَلْيَتَوَكَّلِ
الْمُؤْمِنُونَ ﴿12﴾ * وَلَقَدْ أَخَذَ اللَّهُ مِيثَٰقَ بَنِيٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ربع
وَبَعَثْنَا مِنْهُمُ اثْنَيْ عَشَرَ نَقِيبًا وَقَالَ اللَّهُ إِنِّي مَعَكُمْ
لَئِنْ أَقَمْتُمُ الصَّلَوٰةَ وَءَاتَيْتُمُ الزَّكَوٰةَ وَءَامَنتُم بِرُسُلِي
وَعَزَّرْتُمُوهُمْ وَأَقْرَضْتُمُ اللَّهَ قَرْضًا حَسَنًا لَّأُكَفِّرَنَّ
عَنكُمْ سَيِّـَٔاتِكُمْ وَلَأُدْخِلَنَّكُمْ جَنَّٰتٍ تَجْرِي مِن
تَحْتِهَا الْأَنْهَٰرُ فَمَن كَفَرَ بَعْدَ ذَٰلِكَ مِنكُمْ فَقَدْ
ضَلَّ سَوَآءَ السَّبِيلِ ﴿13﴾ فَبِمَا نَقْضِهِم مِّيثَٰقَهُمْ
لَعَنَّٰهُمْ وَجَعَلْنَا قُلُوبَهُمْ قَٰسِيَةً يُحَرِّفُونَ الْكَلِمَ
عَن مَّوَاضِعِهِۦ وَنَسُوا حَظًّا مِّمَّا ذُكِّرُوا بِهِۦ وَلَا تَزَالُ
تَطَّلِعُ عَلَىٰ خَآئِنَةٍ مِّنْهُمْ إِلَّا قَلِيلًا مِّنْهُمْ فَاعْفُ
عَنْهُمْ وَاصْفَحْ إِنَّ اللَّهَ يُحِبُّ الْمُحْسِنِينَ ﴿14﴾

11. Waɗanda suka ƙafirta suka ƙaryata ayoyi-nmu, waɗancananka sune "yan wuta.

12. Ya waɗanda suka bada gaskiya, ku tuna ni'imar Ubangiji gareku, zamanin da mutane (ƙuraishu) sukayi nufin su miƙa hannayensu) izuwa gareku (donsuyi kisan gilla daku, to, ya kame hannuwansu ga buranku. Kuji tsoron Allah, muminai su dogara bisa Allah.

(WARWAREWAR YAHUDU DA NASARA GA AL-ƘAWURA)

13. Haƙiƙa Ubangiji ya riƙi al-ƙawarin Bani'Isra'ila, mun tsaida shugaba goma sha biyu daga garesu, Ubangiji yace (dasu) haƙiƙa Ni ina taredaku ,(da taimako,) Wallahi idan kun tsaida salla daidai wadaida, kuka bada zakka, kuka bada gaskiya da manzannina, kuka taimake su, kuka rantawa Allah rance kyakkyawa (wato kuka ciyar saboda shi,) Wallahi zan kankare muyagun ayyukanku ga buran ku, Wallahi zan shigar daku aljannatada ƙoramu suke gudana daga ƙarƙashinta, to, wanda ya kafirta daga gareku bayan wancanenka (al-ƙawari,) to, haƙiƙa ya ƙace wa hanyar gaskiya".

14. (Suka warware al-ƙawarin sai Allah yace): "To, saboda warwarewar al-ƙawarinsune muka tsine musu albarka, muka sanya zukatansu ƙeƙasassu suna jirkita kalmomin Attaura (na daga kamannm Manzon Allah tsiran Allah da amincinsa ya tabbata gareshi) ga buran wurarensa. Sun mance rabo da akayi musu gargaɗi dashi (a cikin Attaura,) bazaka gushe bakana tsinkayen ha'inci daga garesu sai kaɗan daga garesu (daga wanda ya Musulunta,) to, sai kai rangwame ga buran su kayi afuwa, haƙiƙa Ubangiji yana son masu kyakkyawan aiki.

وَمِنَ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّا نَصَٰرَىٰٓ أَخَذۡنَا مِيثَٰقَهُمۡ
فَنَسُواْ حَظّٗا مِّمَّا ذُكِّرُواْ بِهِۦ فَأَغۡرَيۡنَا بَيۡنَهُمُ
ٱلۡعَدَاوَةَ وَٱلۡبَغۡضَآءَ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِۚ وَسَوۡفَ
يُنَبِّئُهُمُ ٱللَّهُ بِمَا كَانُواْ يَصۡنَعُونَ ﴿15﴾ يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ
قَدۡ جَآءَكُمۡ رَسُولُنَا يُبَيِّنُ لَكُمۡ كَثِيرٗا مِّمَّا كُنتُمۡ
تُخۡفُونَ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ وَيَعۡفُواْ عَن كَثِيرٖۚ ﴿16﴾
قَدۡ جَآءَكُم مِّنَ ٱللَّهِ نُورٞ وَكِتَٰبٞ مُّبِينٞ ﴿17﴾
يَهۡدِي بِهِ ٱللَّهُ مَنِ ٱتَّبَعَ رِضۡوَٰنَهُۥ سُبُلَ ٱلسَّلَٰمِ
وَيُخۡرِجُهُم مِّنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ بِإِذۡنِهِۦ
وَيَهۡدِيهِمۡ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ﴿18﴾ * لَّقَدۡ كَفَرَ ثمن
ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡمَسِيحُ ٱبۡنُ مَرۡيَمَۚ قُلۡ
فَمَن يَمۡلِكُ مِنَ ٱللَّهِ شَيۡـًٔا إِنۡ أَرَادَ أَن يُهۡلِكَ
ٱلۡمَسِيحَ ٱبۡنَ مَرۡيَمَ وَأُمَّهُۥ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِ
جَمِيعٗاۗ وَلِلَّهِ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَاۚ
يَخۡلُقُ مَا يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ﴿19﴾

15. Akwai waɗanda sukace su Nasarane, to, mun karɓi al-ƙawarinsu (tamfar da muka kara ga bani Isra'ila) to, suka mance rabo daga abinda aka gadar dasu (a cikin Injila, na daga Imani da waninsa suka warware al-ƙawarin,) muka aukar da adawa da ƙiyayya a tsakaninsu izuwa ranar Al-Ƙiyama. Da sannu Allah zai basu Labarin abinda suke aikatawa.

(ALƘUR'ANI DA ABINDA AHALUL - KITABI SUKE BOYEWA)

16. Ya mazowa Littafi! haƙiƙa Manzanmu (tsiran Allah da amincinsa ya tabbata a gareshi) yazo mukuda abinda kuke ƙoyewa na Attaura da Injila, yana rangwame da yawaici (daga wancananka bai bayyana shi ba don ba wata masalaha a ciki sai kunyatar ku kawai).
17. Haƙiƙa haske daga Ubangiji yazo muku (shine Annabi tsiran Allah da amincinsa su tabbata a gareshi) da Littafi mai bayyanawa (shine Al-Ƙur'ani).
18. Allah yana shiriyar wanda yabi yardarsa da wannan Littafi (shine yayi imani, hanyoyin tsira kuma yana fitar dasu daga duffan kafirci izuwa hasken imani, yana shiriyarsu izuwa tafarki madaidaici (Dinil - Islami).

(MUNAƘASHAR NASARA A CIKIN ƘUDIRE -ƘUDIRENSU)

19. Haƙiƙa waɗanda sukace; "Ubangiji shine Masihu ɗan Maryamu" sun kafirta, (wata jama'a ce da akece dasu Yaƙubawa) Cenc "To, wanene ya mallaki wani abu (na ije azabar Allah,) in Ubangiji yanufi ya hallakar da Masihu da mahaifiyarsa da wanda yake cikin ƙasa bakiɗaya?" (Ba wanda ya mallaki wannan mulkin) sammai da ƙassai naga Ubangiji da abinda yake tsakaninsu, Yana halittar abinda yaga dama, Allah mai ikone bisa kowane abu daya nufe shi.

وَقَالَتِ اِ۬لْيَهُودُ وَالنَّصَٰرَيٰ نَحْنُ أَبْنَٰٓؤُاْ اُ۬للَّهِ وَأَحِبَّٰٓؤُهُۥۖ
قُلْ فَلِمَ يُعَذِّبُكُم بِذُنُوبِكُمۖ بَلْ أَنتُم بَشَرٞ مِّمَّنْ خَلَقَۖ يَغْفِرُ لِمَن يَشَآءُ
وَيُعَذِّبُ مَن يَشَآءُۖ وَلِلَّهِ مُلْكُ اُ۬لسَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا
وَإِلَيْهِ اِ۬لْمَصِيرُۖ ﴿20﴾ يَٰٓأَهْلَ اَ۬لْكِتَٰبِ قَدْ جَآءَكُمْ رَسُولُنَا
يُبَيِّنُ لَكُمْ عَلَيٰ فَتْرَةٖ مِّنَ اَ۬لرُّسُلِ أَن تَقُولُواْ مَا جَآءَنَا
مِنۢ بَشِيرٖ وَلَا نَذِيرٖ فَقَدْ جَآءَكُم بَشِيرٞ وَنَذِيرٞۖ
وَاللَّهُ عَلَيٰ كُلِّ شَيْءٖ قَدِيرٞۖ ﴿21﴾ وَإِذْ قَالَ مُوسَيٰ لِقَوْمِهِۦ يَٰقَوْمِ
اِ۟ذْكُرُواْ نِعْمَةَ اَ۬للَّهِ عَلَيْكُمْ إِذْ جَعَلَ فِيكُمْ أَنۢبِيَٰٓءَ وَجَعَلَكُم
مُّلُوكاٗ وَءَاتَيٰكُم مَّا لَمْ يُوتِ أَحَداٗ مِّنَ اَ۬لْعَٰلَمِينَۖ ﴿22﴾ يَٰقَوْمِ
اِ۟دْخُلُواْ اُ۬لْأَرْضَ اَ۬لْمُقَدَّسَةَ اَ۬لتِے كَتَبَ اَ۬للَّهُ لَكُمْۖ وَلَا تَرْتَدُّواْ
عَلَيٰٓ أَدْبَارِكُمْ فَتَنقَلِبُواْ خَٰسِرِينَۖ ﴿23﴾ قَالُواْ يَٰمُوسَيٰٓ إِنَّ فِيهَا
قَوْماٗ جَبَّارِينَۖ وَإِنَّا لَن نَّدْخُلَهَا حَتَّيٰ يَخْرُجُواْ مِنْهَاۖ فَإِن يَخْرُجُواْ
مِنْهَا فَإِنَّا دَٰخِلُونَۖ ﴿24﴾ ۞قَالَ رَجُلَٰنِ مِنَ اَ۬لذِينَ يَخَافُونَ أَنْعَمَ اَ۬للَّهُ
عَلَيْهِمَا اَ۟دْخُلُواْ عَلَيْهِمُ اُ۬لْبَابَۖ فَإِذَا دَخَلْتُمُوهُ فَإِنَّكُمْ
غَٰلِبُونَۖ وَعَلَي اَ۬للَّهِ فَتَوَكَّلُوٓاْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَۖ ﴿25﴾

حزب

20. Yahudu da Nasara sukace (wato kowane ɗaya daga cikinsi yace); "Mu "ya"yan Allah ne (wai kamar "ya"yansa muke cikin kusanci, shi kuma kama uba yake a cikin jinƙai da tausayi,) kuma mu masoyansa ne Cene (dasu Ya Annabi tsiran Allah da amincinsa ya tabbata a gareka,) "To, donme yake muku azabada zunubanku (ubaya azabci ɗansa ko kuwa masoyi ya azabci masoyinsa?) Haba! ku dai mutane ne daga jumlar abinda Allah ya halitta, yana gafara ga wanda yaga dama yana azaba ga wanda yaga dama (ba ace masa donme !) Mulkin sammai da ƙassai yana ga Allah da abinda yake tsakaninsu, makoma tana gareshi,

(TABBATAR DA MANZANCIN ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

21. Yaku mazowa Littafi, haƙiƙa manzanmu yazo muku (Annabi tsiran Allah da amincinsa ya tabbata a gareshi,) yana bayyana muku shari'o'in addini, a bisa yankewa daga manzanni (babu wani manzo tsakaninsa da Annabi Isa sai Annabi khalidu ɗan Sinanu Al-Himyari, wanda mutanen sa basu bada gaskiya dashi ba harsai bayan daya rasu-sanjiy muddar tsakaninsu da Annabi Isa shekara ɗari biyar da sittin [1] don kadaku ,ce (idan an yi muku azaba) "Ba wani mai albishir dayazo mana ko mai gargaɗi", haƙiƙa mai albishir da gargaɗi yazo muku (bakuda hanzari) Allah mai iko ne bisa komai.

(WANI ABU NA DAGA MATSAYAN YAHUDAWA A TAREDA ANNABI MUSA 'ALAIHISSALAMU'),

22. Ka ambata zamanin da Annabi Musa (Alaihissalamu) yake faɗa ga mutanensa, "Yaku mutanena ku tuna ni'imar Ubangiji a gareku, zamanin dayasanya Annabawa a cikinku, yasanya ku sarakuna, ya baku abinda bai baiwa ɗaya daga talikai ba (mannu da tsuntsu salwa da kecewar kogi da wanin wannan).
23. "Yaku mutanena ku shiga ƙasa abar tsarkakewa wadda Allah ya alƙawarta muku (Itace Sham) kadaku ,juya a kan bayayyakinku sai ku zama taɓaɓɓu".
24. Sukace, "ya Musa haƙiƙa cikinta akwai mutane jabberai (Adawa dogwaye masu karfi) haƙiƙa mu bazamu shige ta ba sai sun fita daga cikinta, idan sun fita daga cikinta, to, haƙiƙa mu masu shiga ne cikinta".
25. Maza biyu suka faɗa daga waɗanda suke jin tsoron Allah (Yusha'u da Kalibu 'Alaihimus-salamu') daga zaɓaɓɓun da Annabi Musa (Alaihissalamu) ya aiko na yaye halin jabberai) da Allah yayi ni'ima a garesu (da hanuwa ga buran saɓonsa, Sukace, "Ku shiga ƙofar gari a kansu (ku hana su fitowa,) to, idan kuka shige shi, to, haƙiƙa kune masu galaba, (Sun faɗi wannan don tabbatarwarsu da taimakon Allah a garesu) ku dogara bisa Allah in kun kasance muminai".

1) - Sanajy -

قَالُواْ يَٰمُوسَىٰٓ إِنَّا لَن نَّدْخُلَهَآ أَبَدًا مَّا دَامُواْ فِيهَا فَاذْهَبْ أَنتَ
وَرَبُّكَ فَقَٰتِلَآ إِنَّا هَٰهُنَا قَٰعِدُونَ ﴿26﴾ قَالَ رَبِّ إِنِّي
لَآ أَمْلِكُ إِلَّا نَفْسِي وَأَخِي فَافْرُقْ بَيْنَنَا وَبَيْنَ الْقَوْمِ
الْفَٰسِقِينَ ﴿27﴾ قَالَ فَإِنَّهَا مُحَرَّمَةٌ عَلَيْهِمْ أَرْبَعِينَ سَنَةً
يَتِيهُونَ فِي الْأَرْضِ فَلَا تَأْسَ عَلَى الْقَوْمِ الْفَٰسِقِينَ ﴿28﴾ وَاتْلُ
عَلَيْهِمْ نَبَأَ ابْنَيْ ءَادَمَ بِالْحَقِّ إِذْ قَرَّبَا قُرْبَانًا فَتُقُبِّلَ مِنْ أَحَدِهِمَا
وَلَمْ يُتَقَبَّلْ مِنَ الْآخَرِ قَالَ لَأَقْتُلَنَّكَ قَالَ إِنَّمَا يَتَقَبَّلُ اللَّهُ
مِنَ الْمُتَّقِينَ ﴿29﴾ لَئِنۢ بَسَطتَّ إِلَيَّ يَدَكَ لِتَقْتُلَنِي مَا أَنَا
بِبَاسِطٍ يَدِيَ إِلَيْكَ لِأَقْتُلَكَ إِنِّي أَخَافُ اللَّهَ
رَبَّ الْعَٰلَمِينَ ﴿30﴾ إِنِّي أُرِيدُ أَن تَبُوأَ بِإِثْمِي وَإِثْمِكَ فَتَكُونَ
مِنْ أَصْحَٰبِ النَّارِ وَذَٰلِكَ جَزَٰٓؤُاْ الظَّٰلِمِينَ ﴿31﴾ فَطَوَّعَتْ لَهُ
نَفْسُهُ قَتْلَ أَخِيهِ فَقَتَلَهُ فَأَصْبَحَ مِنَ الْخَٰسِرِينَ ﴿32﴾ فَبَعَثَ اللَّهُ
غُرَابًا يَبْحَثُ فِي الْأَرْضِ لِيُرِيَهُ كَيْفَ يُوَٰرِي سَوْءَةَ أَخِيهِ
قَالَ يَٰوَيْلَتَىٰٓ أَعَجَزْتُ أَنْ أَكُونَ مِثْلَ هَٰذَا الْغُرَابِ
فَأُوَٰرِيَ سَوْءَةَ أَخِي فَأَصْبَحَ مِنَ النَّٰدِمِينَ ﴿33﴾

26. Suka ce"Ya Musa mu haƙiƙa bazamu shige ta ba har abada muddin suna cikinta, sai ka tafi kai da ɗan'uwanka (wan ka) sai ku yake su, haƙiƙa mu muna nan a zaune".
27. Sai Annabi Musa Tsiran Allah da amincinsa su tabbata a gareshi) yace; "Ya Ubangijina ni ban mallaki komai ba sai kaina da ɗan'uwana, sai ka rabe hu-kunci tsakanina da mutane fasiƙai".
28. Ubangiji (Subuhanahu wata'ala) yace (dashi,) "To, ita (wannan ƙasa mai tsarki) abar haramtawa ce a kansu (bazasu shigeta ba,) shekara arba'in, za suyi dimu-wa a cikin ƙasa (mai faɗin far-sahi tara, da tsawon farsahi tala-tin,) kadakai baƙin ciki a bisa mutane fasiƙai. (An ruwa ito cewa suna ta tafiya da dare garjan, in sun wayi gari saisu gansu a wurin da suka fara tafiya, kuma saisu tafi da rana garjan in dare yayi saisu gansu a wurin da suka fara har suka ƙare dukkansu sai kaɗan, wanda bai kai shekara ashirin ba, su dubu ɗari shida ne, da Annabi Musa da Annabi Haruna 'Alaihimussalatu wassalamu' suka mutu a jejin dimuwa aka annabtar da Yusha'u bayan shekara arba'in aka umarce shi dayaƙin jabberan, ya tafi da waɗanda suka ragu tare dashiya yaƙe su ranar Juma'a,aka tsayar masa da rana sa'a guda don yagama yaƙarsu).

(FARKON KASHASSHE A DUNIYA) [1]

29. Ka karanta musu (ya Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wa sallama) Labarin "ya" ya guda biyu na Annabi Adamu 'Alaihissalamu' Habila As said da ƙabila Ashshaki, karanta musu shi) da gaskiya zamanin da suka kusanta hadayarsu izuwa Allah (hadayar rago na habila da sadakar hatsi na ƙabila,) aka ƙarbadaga ɗayansu, (shine Habila shine wuta ta sauko daga sama ta cinye hadayarsa,) ba a karɓa daga ɗayan ba (shine ƙabila, yayi fushiya ɓoye hassada a ransa har izuwa Lokacin da Annabi Adamu ya tafi hajji,) sai yace (da Habila) "Lallai zan kashe ka" (sai yace dashi "Donme , sai yace don an karɓi hadayarka ba a Karɓi tawa ba,)" Sai yace, "Haƙiƙa Allah yana karɓa daga masu jin tsoronsa ne kawai.
30. "Wallahi in ka miƙa hannunka izuwa gareni donka kashe ni ni bazan miƙa hannuna izuwa gareka don in kashe ka ba. Ni ina jin tsoron Allah Ubangijin talikai.
31. "To, haƙiƙa ni ina nufin ka koma da zunubina da zunubinka (wanda kayi tun kafin kisana,) ka zamo cikin "yan wuta, (wancananka sune sakamakon azza-lumai).
32. To, sai ran ƙabila ta riya masa kisan dan'uwansa (Habila) saiya kashe shi, saiya zama daga cikin taɓaɓɓu (bai san yaddazaiyi dashi ba, don shine farkon kashasshe a bayan ƙasa daga bani - Adama, saiya ɗauke shi a gadon bayansa).
33. Sai Allah ya aiko wani hankaka yana tono a cikin ƙasa (da kafafuwansa da bakinsa saboda wani hankaka daya mutu dazai rufe shi,) donya nuna masa yaddazai suturce gawar ɗan uwansa, yace, "Ya kaitona! na gaza in kasance misalin wannan hankaka, in suturce gawar ɗan uwana!' Saiya zama yana mai nadama (a kan daukarsa yayi haka ya binne shi).

1) Wanda yakunshi wanda ya sunnanta sunna kyaky kyewa ladanta na gareshi da wanda ya aikata har Izuwa ranar Alƙiyama da shu'umin hassada

ثمن

* مِنْ أَجْلِ ذَٰلِكَ كَتَبْنَا عَلَىٰ بَنِيٓ إِسْرَآءِيلَ أَنَّهُۥ مَن قَتَلَ نَفْساً
بِغَيْرِ نَفْسٍ اَوْ فَسَادٍ فِي اِ۬لْأَرْضِ فَكَأَنَّمَا قَتَلَ اَ۬لنَّاسَ
جَمِيعاً وَمَنْ أَحْيَاهَا فَكَأَنَّمَا أَحْيَا اَ۬لنَّاسَ جَمِيعاً
وَلَقَدْ جَآءَتْهُمْ رُسُلُنَا بِالْبَيِّنَٰتِ ثُمَّ إِنَّ كَثِيراً مِّنْهُم بَعْدَ ذَٰلِكَ
فِي اِ۬لْأَرْضِ لَمُسْرِفُونَ (34) إِنَّمَا جَزَٰٓؤُاْ اُ۬لَّذِينَ يُحَارِبُونَ
اَ۬للَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَيَسْعَوْنَ فِي اِ۬لْأَرْضِ فَسَاداً اَن يُقَتَّلُوٓاْ
أَوْ يُصَلَّبُوٓاْ أَوْ تُقَطَّعَ أَيْدِيهِمْ وَأَرْجُلُهُم مِّنْ خِلَٰفٍ
أَوْ يُنفَوْاْ مِنَ اَ۬لْأَرْضِ ذَٰلِكَ لَهُمْ خِزْيٌ فِي اِ۬لدُّنْيَا
وَلَهُمْ فِي اِ۬لْأٓخِرَةِ عَذَابٌ عَظِيمٌ (35) إِلَّا اَ۬لَّذِينَ تَابُواْ
مِن قَبْلِ أَن تَقْدِرُواْ عَلَيْهِمْ فَاعْلَمُوٓاْ أَنَّ اَ۬للَّهَ
غَفُورٌ رَّحِيمٌ (36) يَٰٓأَيُّهَا اَ۬لَّذِينَ ءَامَنُواْ اُ۪تَّقُواْ اُ۬للَّهَ
وَابْتَغُوٓاْ إِلَيْهِ اِ۬لْوَسِيلَةَ وَجَٰهِدُواْ فِي سَبِيلِهِۦ
لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ (37) إِنَّ اَ۬لَّذِينَ كَفَرُواْ لَوَ اَنَّ لَهُم
مَّا فِي اِ۬لْأَرْضِ جَمِيعاً وَمِثْلَهُۥ مَعَهُۥ لِيَفْتَدُواْ بِهِۦ مِنْ عَذَابِ
يَوْمِ اِ۬لْقِيَٰمَةِ مَا تُقُبِّلَ مِنْهُمْ وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ (38)

34. Saboda wancananka (abinda ƙabila ya aikata) muka rubuta a kan Bani'Isra'ila cewa haƙiƙa wanda ya kashe kai bada wani kai daya kashe ba, yayi ɓarna a cikin kasa, (shine kifirci ko zina ko fashi da sauransu,) to, kamar ya kashe mutane ne bakidaya, wanda ya raya ta (shine bai kashe kowa ba,) to, kamar ya raya mutane ne bakidaya. haƙiƙa manzanninmu sun zo musu da mu'ujizozi, sannan haƙiƙa yawaici daga garesu bayan wancananka Lallai maɓamata ne a bayanƙasa.

(HUKUNCIN MASUYIN FASHI "MAFASA" WANDA ZARTADDASHINE KADAI ZAI GYARA DUNIYA) [1]

'Yayin da ƙuranawa sukazo Madina alhali basu da Lafiya, Annabi Sallallahu alaihi wasallama yayi musu izini su fita izuwa ra ƙumansa su sha daga bawalantada nononta, yayin da suka sha suka warke, sai suka kashe makiyayin Annabi Sallallahu alaihi wasallama suka kore ra ƙuma) sai Allah yace):

35. Haƙiƙa sakamakon waɗanda suke yaƙi da Allah da manzonsa, suke barna a bayan ƙasa (da fashi,) a karkashe su, ko a tsire su, ko a yanyanke hannayen su da kafafuwansu abar saɓawa, (hannuwan dama da ƙafafuwan hagu,) ko a kore su daga ƙasa, to, wannan sakamako, kunya na garesu a duniya a lahira ma kuma suna da Azaba maigirma [2].

36. Sai waɗanda suka tuba (daga fashi,) tun gaban bakuyi iko a ƙansu ba to, ku sani cewa haƙiƙa Allah mai gafara ne (a garesu mai jinkai (dasu).

(ASALIN TSIRA A LAHIRA) [2]

37. Yaku waɗanda suka bada gakiya, kuji tsoron Allah ku nemi tsanantuwa izuwa gareshi (da abindazai kusanta ku izuwa gareshi na daga ɗa'a, bin umarni, nisantar hani, son Annabawa, son waliyyai, da karɓar wuridinsu, da yawan sadaka, da ziyarar masu ƙaunar Allah, da yawan addu'a, da sadar da zu-munta, da yawaita zikiri da sauransu, kada a kula da masu kafirta Musulmi saboda ziyarar waliyyai, suna cewa wai ziyararsu bautar wanin Allah ne, ba haka ba ne, ziyararsu ƙaunar Allah ce, duba "Sawi" da "tajuttafasiri na shaihu mirgani). Kuyi yaƙi cikin inganta addininsa don ku sami rabauta.

38. Haƙiƙa waɗanda suka kafirtada abinda yake cikin ƙasa baki ɗayaya tabbata garesu da misalinsa tare dashi, donsuyi fansa dashi, daga azabar ranar Alƙiyama! baza a karɓa daga garesu ba, azaba mai raɗaɗi na garesu.

1) Ji tsoron sakamakon magun mutum wandaka kyautata masa.

2) Da mutane sun tsaida kisasi kamar yadda Allah yace a cikin alRur' ani, da duk duniya saita gyaru. Amma tsabar horo da mujarradin tuna-nin mutanen zamani bazai Kara komai ba sai Barna (wato konsutoshin).

3) Asaliw tsira alahira wacce ta kuneshi tsorkan Allah tareda neman shaihi mai shin yarwa izuwa Allah.

يُرِيدُونَ أَن يَخْرُجُوا مِنَ النَّارِ وَمَا هُم بِخَارِجِينَ
مِنْهَا وَلَهُمْ عَذَابٌ مُّقِيمٌ ﴿39﴾ وَالسَّارِقُ وَالسَّارِقَةُ
فَاقْطَعُوا أَيْدِيَهُمَا جَزَاءً بِمَا كَسَبَا نَكَالًا مِّنَ اللَّهِ
وَاللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿40﴾ فَمَن تَابَ مِن بَعْدِ ظُلْمِهِ وَأَصْلَحَ
فَإِنَّ اللَّهَ يَتُوبُ عَلَيْهِ إِنَّ اللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿41﴾ أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ
اللَّهَ لَهُ مُلْكُ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ يُعَذِّبُ مَن يَشَاءُ
وَيَغْفِرُ لِمَن يَشَاءُ وَاللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ﴿42﴾ ۞ يَا أَيُّهَا ربع
الرَّسُولُ لَا يَحْزُنكَ الَّذِينَ يُسَارِعُونَ فِي الْكُفْرِ
مِنَ الَّذِينَ قَالُوا آمَنَّا بِأَفْوَاهِهِمْ وَلَمْ تُؤْمِن قُلُوبُهُمْ
وَمِنَ الَّذِينَ هَادُوا سَمَّاعُونَ لِلْكَذِبِ سَمَّاعُونَ لِقَوْمٍ
آخَرِينَ لَمْ يَأْتُوكَ يُحَرِّفُونَ الْكَلِمَ مِن بَعْدِ مَوَاضِعِهِ
يَقُولُونَ إِنْ أُوتِيتُمْ هَٰذَا فَخُذُوهُ وَإِن لَّمْ تُؤْتَوْهُ فَاحْذَرُوا
وَمَن يُرِدِ اللَّهُ فِتْنَتَهُ فَلَن تَمْلِكَ لَهُ مِنَ اللَّهِ شَيْئًا
أُولَٰئِكَ الَّذِينَ لَمْ يُرِدِ اللَّهُ أَن يُطَهِّرَ قُلُوبَهُمْ
لَهُمْ فِي الدُّنْيَا خِزْيٌ وَلَهُمْ فِي الْآخِرَةِ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿43﴾

39. Suna nufin su fita daga wuta, su ba masu fita ne daga cikinta ba, azaba madauwamiya na garesu.

(SATADA SAKAMAKONTA)

40. Barawo da barauniya, ku yanke hannayensu (na daman kowanne daga cikinsu daga mađun buran hannu in sun saci mbu'in dinare da abinda yayi sama,) sakamako na abinda suka aikata, ban kashi daga Allah, Allah mabuwayi ne gwanine (a cikin halitta dayasanya wannan sak-amako mai tasiri a cikin rage yađuwar sata. Da ana aikatawa kamar yadda Allah ya fada, da sata bata yađu ba, mutanen yamma sun ƙagi hukuncc hukuncensu, bana Wahayin sama ba, saboda haka babu abindazai auku a bayan ƙasa sai karin ɓarna).

41. To, wanda ya tuba bayan zaluncinsa, ya kyautata aikinsa to, haƙiƙa Allah zai karɓi tubansa, haƙiƙa Ubangiji mai đimbin ga-fara ne da jinƙai.

42. Ai kasani, haƙiƙa Allah mulkin sammai da ƙassaina gareshi, yana azaba ga wanda yaga dama yana gafara ga wanda yaga dama, Allah mai iko ne bisa komai

(YAHUDU DA MATSAYINSU DAGA HUKUNCE-HUKUNCEN ATTAURA)

43. Ya kai manzo, kada wađanda suke gaggawa a cikin kafirci su bakanta maka, sune wađanda Sukace, mun bada gaskiya da harasansu, alhali zuciyoyinsu bata bada gakiya ba, (munafukai,) akwai daga yahudawa mutane masu yawan saurarон ƙarya, masu yawan sauraro đon wađansu mutane daban (na Yahudu,) da basu zo maka ba, (sune mutanen Haibara, wađansu katangantattu daga cikinsu sukayi zina.basu jefe su basuka aiko ƙuraizatu donsuji hukuncin wađannan mutane,) suna jirkita kalmomin dasuke cikin Attaura (kamar ayar rajamu,) bayan guraransa (da Allah ya ajiye ta a kanta,) suna cewa (ga wađanda suka aika,) "In an baku wannan (hukunci jirkitaccen nan wato idan Annabi yayi muku fatawa dashi,) to, ku karɓe shi, idan ko ba a baku shi ba, kuji tsoron karɓa". Wanđa Allah yanufi ɓatar dashi, to, bazaka mallaki wani abu badaga Allah (a cikin ije masa fitina) ba, wađancananka su ne wađanda Allah bai nufi ya tsarkake zukatansu ba (daga kafirci,) kunya na garesu a duniya, azaba maigirma na garesu a Lahira.

سَمَّٰعُونَ لِلۡكَذِبِ أَكَّٰلُونَ لِلسُّحۡتِۚ فَإِن جَآءُوكَ
فَٱحۡكُم بَيۡنَهُمۡ أَوۡ أَعۡرِضۡ عَنۡهُمۡۖ وَإِن تُعۡرِضۡ عَنۡهُمۡ
فَلَن يَضُرُّوكَ شَيۡـٔٗاۖ وَإِنۡ حَكَمۡتَ فَٱحۡكُم بَيۡنَهُم بِٱلۡقِسۡطِۚ
إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُقۡسِطِينَ ﴿44﴾ وَكَيۡفَ يُحَكِّمُونَكَ وَعِندَهُمُ
ٱلتَّوۡرَىٰةُ فِيهَا حُكۡمُ ٱللَّهِ ثُمَّ يَتَوَلَّوۡنَ مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَۖ وَمَآ
أُوْلَٰٓئِكَ بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ ﴿45﴾ إِنَّآ أَنزَلۡنَا ٱلتَّوۡرَىٰةَ فِيهَا هُدٗى وَنُورٞۖ
يَحۡكُمُ بِهَا ٱلنَّبِيٓـُٔونَ ٱلَّذِينَ أَسۡلَمُواْ لِلَّذِينَ هَادُواْ
وَٱلرَّبَّٰنِيُّونَ وَٱلۡأَحۡبَارُ بِمَا ٱسۡتُحۡفِظُواْ مِن كِتَٰبِ ٱللَّهِ
وَكَانُواْ عَلَيۡهِ شُهَدَآءَۚ فَلَا تَخۡشَوُاْ ٱلنَّاسَ وَٱخۡشَوۡنِۖ
وَلَا تَشۡتَرُواْ بِـَٔايَٰتِي ثَمَنٗا قَلِيلٗاۚ وَمَن لَّمۡ يَحۡكُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ
فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡكَٰفِرُونَ ﴿46﴾ ۞ وَكَتَبۡنَا عَلَيۡهِمۡ فِيهَآ ثمن
أَنَّ ٱلنَّفۡسَ بِٱلنَّفۡسِ وَٱلۡعَيۡنَ بِٱلۡعَيۡنِ وَٱلۡأَنفَ بِٱلۡأَنفِ
وَٱلۡأُذۡنَ بِٱلۡأُذۡنِ وَٱلسِّنَّ بِٱلسِّنِّ وَٱلۡجُرُوحَ قِصَاصٞۚ
فَمَن تَصَدَّقَ بِهِۦ فَهُوَ كَفَّارَةٞ لَّهُۥۚ وَمَن لَّمۡ
يَحۡكُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿47﴾

44. Su masu yawan sauraron ƙarya ne, masu yawan cin haram ne, to, idan sukazo maka (don kai hukunci tsakaninsu,) sai kai hukunci tsakaninsu ko ka bujire ga buransu , (wannan zaɓin abin shafewa ne da faɗin Ubangiji WA'AN AHKUM BAINAHUM) idan ka bujere ga buran su, to, basu cuce ka komai ba idan kayi hukunci tsakaninsu to yi hukunci tsakaninsu da adalci, haƙiƙa Ubangiji yana son masu hukunci da adalci.

45. Yaya zasu sarautaka, ga Attaura a wurinsu wacce hukuncin Allah yake cikinta (na rajamu,) sannan su bada baya bayan wancananka sarautarwar nan? Waɗancananka ba muminai ne ba.

AKWAI HUKUNCIN ALLAH A CIKIN TTAURA AMMA YAHUDAWA SUN BUJIRE GA BURAN TA)

46. Haƙiƙa mu mun saukar da Attaura shiriya (daga ɓata) da bayanin hukunce -hukunce, Annabawa na Bani' Isra'ila suna hukunci da ita, waɗanda suka jawu ga Allah, ga waɗannan da suka Yahudanta, da masana daga cikinsu, da faƙihansu, saboda an kiyayar dasu Littafin Allah, sun kasance shaidu a kansa (cewa gaskiya ne,) to, kadaku ,ji tsoron mutane, (a cikin bayyana abinda yake gareku na daga bayanin sufofin Manzon Allah da rajamu, da waninsa,) kuji tsorona (a cikin ɓoye shi,) kadaku ,canja ɗan tamani ƙanƙane maimakon ayoyi-na, wanda bai yi hukunci da abinda Allah ya saukar ba to, waɗancananka sune kafirai (wato tsagaggu).

47. Mun wajabta a garesu a cikin Attaura, haƙiƙa kai ana kashe tada kisan kai, idanu ana cire tada cire ido, hanci ana gutsire shi da gutsire hanci, kunne ana yanke ta dayanke kunne, haƙori ana .cire tada cire haƙori, miyaku ana yin ƙisasi cikinta (idan yayiwu, kamar hannu da ƙafa da sauransu,) to, wanda yayi sadaka da ƙisasi (shine ya miƙo kansa ga ƙisasi,) to, shi ƙisasin nan kaffara ce gareshi. Wanda bai yi hukunci da abinda Allah ya saukar ba (a cikin ƙisasi da waninsa,) to, waɗancananka sune azzalumai.

وَقَفَّيْنَا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم بِعِيسَى ٱبْنِ مَرْيَمَ مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ
مِنَ ٱلتَّوْرَىٰةِ وَءَاتَيْنَٰهُ ٱلْإِنجِيلَ فِيهِ هُدًى وَنُورٌ وَمُصَدِّقًا لِّمَا
بَيْنَ يَدَيْهِ مِنَ ٱلتَّوْرَىٰةِ وَهُدًى وَمَوْعِظَةً لِّلْمُتَّقِينَ ﴿48﴾ وَلْيَحْكُمْ
أَهْلُ ٱلْإِنجِيلِ بِمَا أَنزَلَ ٱللَّهُ فِيهِ وَمَن لَّمْ يَحْكُم بِمَا أَنزَلَ ٱللَّهُ
فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْفَٰسِقُونَ ﴿49﴾ وَأَنزَلْنَآ إِلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ
بِٱلْحَقِّ مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ مِنَ ٱلْكِتَٰبِ وَمُهَيْمِنًا عَلَيْهِ
فَٱحْكُم بَيْنَهُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ وَلَا تَتَّبِعْ أَهْوَآءَهُمْ عَمَّا جَآءَكَ
مِنَ ٱلْحَقِّ لِكُلٍّ جَعَلْنَا مِنكُمْ شِرْعَةً وَمِنْهَاجًا
وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ لَجَعَلَكُمْ أُمَّةً وَٰحِدَةً وَلَٰكِن لِّيَبْلُوَكُمْ
فِى مَآ ءَاتَىٰكُمْ فَٱسْتَبِقُوا۟ ٱلْخَيْرَٰتِ إِلَى ٱللَّهِ مَرْجِعُكُمْ جَمِيعًا
فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ فِيهِ تَخْتَلِفُونَ ﴿50﴾ * وَأَنِ ٱحْكُم
بَيْنَهُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ وَلَا تَتَّبِعْ أَهْوَآءَهُمْ وَٱحْذَرْهُمْ
أَن يَفْتِنُوكَ عَنۢ بَعْضِ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ إِلَيْكَ
فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَٱعْلَمْ أَنَّمَا يُرِيدُ ٱللَّهُ أَن يُصِيبَهُم
بِبَعْضِ ذُنُوبِهِمْ وَإِنَّ كَثِيرًا مِّنَ ٱلنَّاسِ لَفَٰسِقُونَ ﴿51﴾

ربع

48. Mun biyar da Annabi Isa ɗan Maryama bisa guraban Anna-bawa (Alaihimussalatu wassala-mu,) mai gasgatawar abinda yake gabansa na Attaura, Munbashi Linjila akwai shiriya (daga ɓata) a cikinsa, da haske (wato bayani na hukunce-hukunce,) mai gasgatawa da abinda yake gabansa na Attaura (na hukunce -hukunce,) dashiriya da gargaɗi ga masu jin tsoron Allah.
49. (Mun ce) "Ma'abota Linjila suyi aiki da abinda aka saukar a cikin Linjila, wanda bai hukunci da abinda Allah ya saukar ba, haƙiƙa waɗancananka sune fasiƙai".

(HUKUNCI DA LITTAFIN ALLAH DA DOKAR ALƘUR'ANI)

50. Mun saukar da Alƙur'ani izuwa gareka da gaskiya, mai gasgatawa da abinda yake gabansa na daga Littafi mai shaida a kansa, sai kayi hukunci tsakanin ahalul-kitabi (in sun kawo ƙara gareka,) da abinda Allah ya saukar izuwa gareka, kadaka bi soyesoyen zukatansu, kana mai ratsewa daga abinda yazo maka na daga gaskiya. Mun sanya shari'a daga kowanne daga garekuda hanya mabayyaniya. Da Allah yaga dama da saiya mai daku ,al'umma ɗaya a kan shari'a ɗaya.sai dai (ya rarrabaku ne) domin ya jarrabaku a cikin abinda ya baku (na daga shari'o'i masu sassabawa don yaga mai bi daga garekuda mai saɓo,) to, kuyi tsereren‌iya na alherai, makoinarkii lana ga Ubangiji bakiɗaya, saiya baku Labarin abinda kuka kasance kuna sassabawa a cikinsa (na daga Lamarin addini).
51. Ka. yi hukunci tsakaninsu da abinda Allah ya saukar, kadaka bi soye - soyen zukatansu, kayi hir dasu kaji tsoron su don kadasu ɓassheka ga buran sashin abinda ya saukar izuwa gareka, to, in sun bada baya (ga buran hukunci da aka saukar maka suka nufi waninsa,) to, ka sani cewa dai haƙiƙa Allah yana nufin yayi musu uƙuba (a nan duniya) da ba'alin zunubansu, (kuma a Lahira yayi musu sakamako a kanta, (To, Musulmi wannan wulakanci daya sami Musulmi a wannan filin duniya, to, ta nan ya same mu, Allah ya maganta, Amin). Haƙiƙa yawaici daga mutane lallai fasiƙai ne.

أَفَحُكْمَ الْجَاهِلِيَّةِ يَبْغُونَ وَمَنْ أَحْسَنُ مِنَ اللَّهِ حُكْمًا
لِّقَوْمٍ يُوقِنُونَ ﴿52﴾ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا لَا تَتَّخِذُوا الْيَهُودَ
وَالنَّصَارَىٰ أَوْلِيَاءَ بَعْضُهُمْ أَوْلِيَاءُ بَعْضٍ وَمَن يَتَوَلَّهُم مِّنكُمْ
فَإِنَّهُ مِنْهُمْ إِنَّ اللَّهَ لَا يَهْدِي الْقَوْمَ الظَّالِمِينَ ﴿53﴾
فَتَرَى الَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٌ يُسَارِعُونَ فِيهِمْ يَقُولُونَ نَخْشَىٰ
أَن تُصِيبَنَا دَائِرَةٌ فَعَسَى اللَّهُ أَن يَأْتِيَ بِالْفَتْحِ
أَوْ أَمْرٍ مِّنْ عِندِهِ فَيُصْبِحُوا عَلَىٰ مَا أَسَرُّوا فِي أَنفُسِهِمْ
نَادِمِينَ ﴿54﴾ يَقُولُ الَّذِينَ آمَنُوا أَهَٰؤُلَاءِ الَّذِينَ أَقْسَمُوا بِاللَّهِ
جَهْدَ أَيْمَانِهِمْ إِنَّهُمْ لَمَعَكُمْ حَبِطَتْ أَعْمَالُهُمْ فَأَصْبَحُوا خَاسِرِينَ ﴿55﴾
يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا مَن يَرْتَدِدْ مِنكُمْ عَن دِينِهِ
فَسَوْفَ يَأْتِي اللَّهُ بِقَوْمٍ يُحِبُّهُمْ وَيُحِبُّونَهُ أَذِلَّةٍ عَلَى الْمُؤْمِنِينَ
أَعِزَّةٍ عَلَى الْكَافِرِينَ يُجَاهِدُونَ فِي سَبِيلِ اللَّهِ وَلَا يَخَافُونَ
لَوْمَةَ لَائِمٍ ذَٰلِكَ فَضْلُ اللَّهِ يُؤْتِيهِ مَن يَشَاءُ
وَاللَّهُ وَاسِعٌ عَلِيمٌ ﴿56﴾ إِنَّمَا وَلِيُّكُمُ اللَّهُ وَرَسُولُهُ وَالَّذِينَ آمَنُوا
الَّذِينَ يُقِيمُونَ الصَّلَاةَ وَيُؤْتُونَ الزَّكَاةَ وَهُمْ رَاكِعُونَ ﴿57﴾

52. Shin to, hukuncin jahiliyya suke nema ne? Babu mafi kyaun hukunci daga Allah ga mutanen da suka sakankance dashi, (a bisa turmuzar hancin shirye - shiryen mutanen yamma).

(DAUKAKAR [1] YAHUDU DA NASARA DA AƘIBARTA)

53. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! ka daku ,riƙi Yahudu da Nasara ababan daukaka, ba'alinsu majuɓuntan ba'ali ne (saboda jiɓintuwa a cikin kafirci,) duk wanda yajiɓince su daga cikinku, to, haƙiƙa yana daga cikinsu, haƙiƙa Allah baya shiriyar mutane azzalumai.

54. Kana ganin waɗanda munafunci yake cikin zuciyarsu, suna garaje a cikin daukakarsu, suna cewa muna tsoron kada musibata same mu ne, (fari ko rinjaye, ya zama Lamarin Annabi Sallallahu alaihi wasallama bai dore basu hana mu abinci, Ubangiji yace): "Ana ƙauna Allah yazoda buɗi ko wani al'amari daga gareshi (taimakon Annabi Sal-lallahu alaihi wasallama da keta asirin munafukai) su zama masu nadama ga abinda suka ɓoye a cikin kawukansu).

55. Waɗanda suka bada gaskiya suna faɗi (ga ba'alinsu yayin da aka keta asiran munafikai suna faɗa saboda mana ki,) "Yanzu waɗancananka, sune waɗanda suka rantse da Allah matukar rantse - rantsen su cewa haƙiƙa su suna taredaku ,(a cikin addini?" Ubangiji yace,) "Aikinsu ya Lalace, sai suka zama taɓaɓɓu (a duniya da kunyata a Lahira da azaba)".

(MURTADDAI DA MASU YAƘARSU) DA AL BISHIR DA AƘIDAR ASH'ARIYA - CIKIN AL KUR'ANI

56. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! wanda yayi ridda daga cikinku ga buran addininsa (wannan Labarin gaibu ne ya afku bayan kaurar Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama) to, da sannu Allah zai zoda mutane da yake sun su suke son sa, (Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama ya nuna Abu Musal'ash'ari yace sune mutanen, Hakimu ya ruwa ito shi a cikin Sahihinsa). Masu jinƙai a kan muminai masu kaushi a kan kafirai, suna yaƙi Fisabilillahi, basa tsoron zargin mai zargi, wancananka (abin ambato na daga sufofi kyawawa,) falalar Allah ce yake bada ita ga wanda yaga dama, Allah mayalwacin falala ne masanine (da wanda ya cancanta. Abdullahi Ibn Salami yace, Ya Rasulullahi mutanan nan sun ƙaurace mana, sai Allah yace):

57. Haƙiƙa Allah da ma'aikinsa sune majiɓuntanku kawai, da waɗanda suka bada gaskiya, waɗanda suke tsayar da salla suke bada zakka alhali suna masu ƙanƙan - da - kai (a cikin sallarsu da bada zakkarsu).

1) Runguma.

وَمَنْ يَتَوَلَّ اَللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَالذِينَ ءَامَنُواْ فَإِنَّ حِزْبَ اَللَّهِ هُمُ
اُلْغَٰلِبُونَ ﴿58﴾ يَٰأَيُّهَا اَلذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّخِذُواْ اُلذِينَ اَتَّخَذُواْ دِينَكُمْ
هُزُؤاً وَلَعِباً مِّنَ اَلذِينَ أُوتُواْ اُلْكِتَٰبَ مِن قَبْلِكُمْ وَالْكُفَّارَ أَوْلِيَآءَ
وَاتَّقُواْ اُللَّهَ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿59﴾ وَإِذَا نَادَيْتُمْ إِلَى اَلصَّلَوٰةِ
اِتَّخَذُوهَا هُزُؤاً وَلَعِباً ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ قَوْمٌ لَّا يَعْقِلُونَ ﴿60﴾ * قُلْ ثمن
يَٰأَهْلَ اَلْكِتَٰبِ هَلْ تَنقِمُونَ مِنَّا إِلَّا أَنْ ءَامَنَّا بِاللَّهِ وَمَا أُنزِلَ
إِلَيْنَا وَمَا أُنزِلَ مِن قَبْلُ وَأَنَّ أَكْثَرَكُمْ فَٰسِقُونَ ﴿61﴾ قُلْ هَلْ
أُنَبِّئُكُم بِشَرٍّ مِّن ذَٰلِكَ مَثُوبَةً عِندَ اَللَّهِ مَن لَّعَنَهُ اُللَّهُ وَغَضِبَ
عَلَيْهِ وَجَعَلَ مِنْهُمُ اُلْقِرَدَةَ وَالْخَنَازِيرَ وَعَبَدَ اَلطَّٰغُوتَ
أُوْلَٰٓئِكَ شَرٌّ مَّكَاناً وَأَضَلُّ عَن سَوَآءِ اِلسَّبِيلِ ﴿62﴾ وَإِذَا جَآءُوكُمْ
قَالُواْ ءَامَنَّا وَقَد دَّخَلُواْ بِالْكُفْرِ وَهُمْ قَدْ خَرَجُواْ بِهِۦ وَاللَّهُ أَعْلَمُ
بِمَا كَانُواْ يَكْتُمُونَ ﴿63﴾ وَتَرَىٰ كَثِيراً مِّنْهُمْ يُسَٰرِعُونَ فِي اِلْإِثْمِ
وَالْعُدْوَٰنِ وَأَكْلِهِمُ اُلسُّحْتَ لَبِئْسَ مَا كَانُواْ
يَعْمَلُونَ ﴿64﴾ لَوْلَا يَنْهَىٰهُمُ اُلرَّبَّٰنِيُّونَ وَالْأَحْبَارُ
عَن قَوْلِهِمُ اُلْإِثْمَ وَأَكْلِهِمُ اُلسُّحْتَ لَبِئْسَ مَا كَانُواْ يَصْنَعُونَ ﴿65﴾

58. Wanda duk yajiɓinci Allah da manzonsa da waɗanda suka bada gaskiya, (ya taimake su,) to, haƙiƙa rundunar Allah sune ainihin masu rinjaye su kaɗai.

(HANI GA BURAN DAUKAKAR KAFIRAI DA DALILI A CIKIN WANNAN)

59. Ya waɗanda suka bada gaskiya! kadaku, riƙi waɗanda suka riƙi addimnku abin izgili (dashi abin wasa (dashi) kadaku ,riƙe su ababan jiɓinta daga waɗanda aka basu Littafi gabankuda mushurukai. Kuji tsoron Allah in kun kasance masu gaskiya (cikin imani).

60. Sune waɗanda idan kun kira su zuwa salla (da kiran salla) saisu riƙeta abin izgili abin wasa (da ita) to, sun riƙeta haka saboda haƙiƙa su mutane ne da basu da hankali.

(GABAR KAFIRAI DA MUSULUNCI TUN DA HAR YANZU HAR IZUWA ALƘIYAMA)

"yayin dayahudawa sukace da Annabi Sallallahu alaihi wasallama; Da wa ka bada gaskiya daga Manzanni, sai yace; Da abinda Allah ya saukar izuwa garemu har ya ambaci Annabi Isa 'Alaihissalamu' sai suka ce; Bamu san addini mafi sharri daga addininku ba. Sai Allah yace":

61. Cene, "Yaku mazowa Littafi, ba kwa kin komai daga garemu sai cewa - mun bada gaskiya da Allah da abinda aka saukar izuwa garemu, da abinda aka saukar daga gabanmu (izuwa Annabawa,) haƙiƙa yawaicinku fasiƙai ne".

62. Cene, (dasu) :Shin bana baku Labari badaga mafi sharri daga mazowa wannan, mafi sharrin makoma nan ga Ubangiji shine wanda Allah ya tsine masa albarka yayi fushi a kansa, yasanya birrai da alhanzirai daga cikinsu, ya bautawa shaiɗan, (sune Yahudu,) waɗancananka sune mafi sharrin mazauni, mafi ɓacewa daga tsattsakin hanyar gaskiya. (Raddi ne Allah yayi musu bisa faɗinsu, bamu san addini mafi sharri daga addininku ba).

63.Idan munafukan Yahudawa sun zo muku, saisu ce mun bada gaskiya, haƙiƙa sun shigo (izuwa gareku) da kafircinsu, kuma alhali sun fita (daga gareku) da kafircinsu, Allah masanine da abinda suka kasance suna ɓoyewa (na daga kafirci).

64. Kana ganin yawaici daga Yahudawa suna garaje a cikin ƙarya da zalunci da cin haram (Kamar rashawa) Lallai abinda suka kasance suna aikatawa ya mugusta.

65. Ɗonme masana Allansu da mal-amansu basu hane su ba gaburan faɗinsu ƙarya da cin su haram, abinda suka kasance suna aikatawa Lallai ya mugusta, (na buran hanin nan).

(WANI ABU DAGA MIYAGUN YAHUDAWA DA HANYAR TSIRA DUNIYA DA LAHIRA)

وَقَالَتِ ٱلْيَهُودُ يَدُ ٱللَّهِ مَغْلُولَةٌ غُلَّتْ أَيْدِيهِمْ وَلُعِنُوا۟ بِمَا قَالُوا۟ۘ
بَلْ يَدَاهُ مَبْسُوطَتَانِ يُنفِقُ كَيْفَ يَشَآءُۚ وَلَيَزِيدَنَّ كَثِيرًا مِّنْهُم
مَّآ أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ طُغْيَٰنًا وَكُفْرًاۚ وَأَلْقَيْنَا بَيْنَهُمُ ٱلْعَدَٰوَةَ
وَٱلْبَغْضَآءَ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِۚ كُلَّمَآ أَوْقَدُوا۟ نَارًا لِّلْحَرْبِ أَطْفَأَهَا ٱللَّهُۚ
وَيَسْعَوْنَ فِى ٱلْأَرْضِ فَسَادًاۚ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿66﴾
وَلَوْ أَنَّ أَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ ءَامَنُوا۟ وَٱتَّقَوْا۟ لَكَفَّرْنَا عَنْهُمْ سَيِّـَٔاتِهِمْ
وَلَأَدْخَلْنَٰهُمْ جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ﴿67﴾ وَلَوْ أَنَّهُمْ أَقَامُوا۟ ٱلتَّوْرَىٰةَ
وَٱلْإِنجِيلَ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيْهِم مِّن رَّبِّهِمْ لَأَكَلُوا۟ مِن فَوْقِهِمْ
وَمِن تَحْتِ أَرْجُلِهِمۚ مِّنْهُمْ أُمَّةٌ مُّقْتَصِدَةٌۖ وَكَثِيرٌ مِّنْهُمْ
سَآءَ مَا يَعْمَلُونَ ﴿68﴾ ۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلرَّسُولُ بَلِّغْ مَآ أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَۖ
وَإِن لَّمْ تَفْعَلْ فَمَا بَلَّغْتَ رِسَالَتَهُۥۚ وَٱللَّهُ يَعْصِمُكَ مِنَ ٱلنَّاسِۗ
إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿69﴾ قُلْ يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ
لَسْتُمْ عَلَىٰ شَىْءٍ حَتَّىٰ تُقِيمُوا۟ ٱلتَّوْرَىٰةَ وَٱلْإِنجِيلَ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيْكُم
مِّن رَّبِّكُمْۗ وَلَيَزِيدَنَّ كَثِيرًا مِّنْهُم مَّآ أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ
طُغْيَٰنًا وَكُفْرًاۖ فَلَا تَأْسَ عَلَى ٱلْقَوْمِ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿70﴾

ربع

66. Yahudawa sukace (yayin da aka ƙuntata a garesu da ƙaryatarwar Annabi dayai musu, bayan sun fi kowa dukiya). Hannun Ubangiji ƙuƙuntacciyace (ga buran sakin alheri a kansu, Ubangiji yace,) 'An ƙuƙunce hannayensu an tsine musu albarka, saboda abin nan da suka faɗa, haba! hannayen Ubangiji a shimfiɗe suke (da zuba alhen badare ba rana,) yana ciyarwa yadda yaga dama, Lallai abinda aka saukar izuwa gareka (Alƙur'ani) yana ƙarawa yawaici daga garesu shisshigi da kafirci (saboda kafircewarsu dashi). Mun jefa ƙiyayya da adawa tsakaninsu har izuwa ranar alƙiyama, (kowace jama'a daga garesu tana ƙin "yar'uwarta, haka ma Mishan suke su ma ba son junansu suke ba) koyaushe suka hura wutar yaƙi (ga Annabi Sallallahu alaihi wasallama,) sai Allah ya biceta, suna ƙoƙari a cikin ƙasa don ɓarna, Allah ba yason masu barna.

67. Da mazowa Littafi zasu bada gakiya da Annabi (Sallallahu alaihi wasallama suji tsoron kafirci da mun kankare miyagun ayyukansu ga buransu, da mun shigar dasu aljannatan jin daɗi.

68. Da cewa su sun tsaida Attaura da Linjila sun yi aiki da abinda yake ciki (gasgata Manzon Allah yana daga ciki) da abinda aka saukar izuwa garesu daga Ubangijinsu na Littattafai dasun ci daga birbishinsu, daga kuma karƙashin kafafuwa (a yalwata musu wajen arziki, a kwarara musu shi ta kowace jiha,) akwai jama'a daga cikinsu masu aiki madai - daici tana aiki dashi (sune waɗanda suka bada gaskiya da Annabi Sallallahu alaihi wasallama kamar Abdullahi Ibn Salami da abokansa) yawaicinsu abinda suke aikatawa ya mugusta.

(WAJAB CIN ISAR DA AIKE)

69. Ya wannan manzo maigirma! iyadda aiken dukkan abinda aka saukar a gareka daga Ubangijinka (kadaka ɓoye wani abu don tsoron kada a same ka da wani abin ƙi,) in baka aikata haka ba, to, baka isar da sakonninsa ba, Allah ne mai kiyaye ka daga sharrin mutane, (Manzon Allah ya kasance ana kiwonsa, yayin da wannan ta sauka, sai yace ku tafi gida, haƙiƙa Allah ya kiyaye ni, Hakimune ya ruwaito wannan hadisi) haƙiƙa Allah baya shiriyar mutane kafirai.

WAJABCIN ƘAN ƘAME AL ƘUR'ANI

70. Cene "Yaku mazowa Littafi, baku kasance a kan komai ba sai kun tsaida Attaura da Linjila da abinda aka saukar daga Ubangijinku, haƙiƙa abinda aka saukar a gareka daga Ubangijinka yana ƙara wa yawaici daga cikinsu shisshigi da kafirci. Ƙadakai baƙin ciki bisa mutane kafirai, jin basu bada gaskiya dakai ba).

إِنَّ الَّذِينَ ءَامَنُواْ وَالَّذِينَ هَادُواْ وَالصَّابُونَ وَالنَّصَٰرَىٰ مَنْ ءَامَنَ
بِاللَّهِ وَالْيَوْمِ الْاخِرِ وَعَمِلَ صَٰلِحاً فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ
وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ (71) لَقَدْ أَخَذْنَا مِيثَٰقَ بَنِي إِسْرَآءِيلَ
وَأَرْسَلْنَا إِلَيْهِمْ رُسُلاً كُلَّمَا جَآءَهُمْ رَسُولٌ بِمَا
لَا تَهْوَىٰ أَنفُسُهُمْ فَرِيقاً كَذَّبُواْ وَفَرِيقاً يَقْتُلُونَ (72)
وَحَسِبُواْ أَلَّا تَكُونَ فِتْنَةٌ فَعَمُواْ وَصَمُّواْ ثُمَّ تَابَ اللَّهُ
عَلَيْهِمْ ثُمَّ عَمُواْ وَصَمُّواْ كَثِيرٌ مِّنْهُمْ وَاللَّهُ بَصِيرٌ
بِمَا يَعْمَلُونَ (73) لَقَدْ كَفَرَ الَّذِينَ قَالُواْ إِنَّ اللَّهَ
هُوَ الْمَسِيحُ ابْنُ مَرْيَمَ وَقَالَ الْمَسِيحُ يَٰبَنِي إِسْرَآءِيلَ اعْبُدُواْ
اللَّهَ رَبِّي وَرَبَّكُمْ إِنَّهُ مَن يُشْرِكْ بِاللَّهِ فَقَدْ حَرَّمَ اللَّهُ
عَلَيْهِ الْجَنَّةَ وَمَأْوَىٰهُ النَّارُ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنْ أَنصَارٍ (74)
لَّقَدْ كَفَرَ الَّذِينَ قَالُواْ إِنَّ اللَّهَ ثَالِثُ ثَلَٰثَةٍ وَمَا مِنْ إِلَٰهٍ
إِلَّا إِلَٰهٌ وَاحِدٌ وَإِن لَّمْ يَنتَهُواْ عَمَّا يَقُولُونَ لَيَمَسَّنَّ
الَّذِينَ كَفَرُواْ مِنْهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ (75) أَفَلَا يَتُوبُونَ
إِلَى اللَّهِ وَيَسْتَغْفِرُونَهُ وَاللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ (76)

71. Haƙiƙa waɗanda suka bada gakiya, Yahudawa da sabawa (masu ridda izuwa wani addinin) da Nasara, wanda ya bada gaskiya daga garesu da Allah da ranar Lahira, yayi aiki nagari to, ba tsoro a garesu, baza suyi baƙin ciki ba (a Lahira).

(WANI ABU DAGA MIYAGUN HALAYEN YAHUDU HAR YAU)

72. Haƙiƙa mun riƙi alƙawarin Bani-Isra'ila da Allah da manzanni, mun aiko jakadu izuwa garesu, kodayaushe jakada daga garesu yazo musu, da abinda ransu bata sha'awa, to, saisu ƙaryata, waɗansu daga cikinsu su kashe waɗansu (kamar Annabi Ya-haya da Zakariya Alaihimussalamu).

73. Suna zaton fitina bazata auku ba (a bisa ƙaryata manzanni da kisan su,) suka makanta (ga buran gaskiya,) suka kurumta (ga buranjinsa,) sannan Ubangiji ya karɓi tuban su, sannan suka makanta suka kurunta (wato) yawaici daga garesu. Allah masanine ga abinda suke aikatawa.

RADDI BISA AƘI DAR. TURAWA WATO (UKUN -TAWA) DA KADAI TAWA

74. Haƙiƙa waɗanda sukace "Ubangiji shine Masihu dan Maryamu" sun kafirta, shi Masihu yace (dasu) "Ya Bani - Isra'ila! ku bautawa Allah, Ubangijina Ubangijinku, (ni bawa ne ba Ubangiji ba ne,) haƙiƙa wanda yayi shirka da Allah lallai Allah ya haramta masa aljanna, makomarsa wuta, azzalumai basu da masu hana musu azaba".

75. Haƙiƙa waƙanda sukace "Allah na ukun uku ne" sun kafirta, (wato Isa da mahaifiyarsa da ran tsarki) Babu wani abin bautawa da gaskiya sai Allah makaɗaicin Sarki, idan basu hanu ga buran abinda suke faɗa ba (na daga ukuntawa,) Lallai azaba mai raɗaɗi zata shafi kafirai daga cikinsu.

76. Shin basa tuba ba ga Allah su nemi gafararsa? Allah mai gafara ne mai jinƙai.

(HALACCIN BIJIRE-BIJIRE NA MUTUNTAKA) HAR YAU

ثمن

۞ مَا اَ۬لْمَسِيحُ اُ۪بْنُ مَرْيَمَ إِلَّا رَسُولٞ قَدْ خَلَتْ مِن قَبْلِهِ اِ۬لرُّسُلُۖ
وَأُمُّهُۥ صِدِّيقَةٞۖ كَانَا يَأْكُلَٰنِ اِ۬لطَّعَامَۖ اُ۟نظُرْ كَيْفَ
نُبَيِّنُ لَهُمُ اُ۬لْءَايَٰتِ ثُمَّ اَ۟نظُرْ أَنَّيٰ يُؤْفَكُونَۖ ﴿77﴾
قُلْ أَتَعْبُدُونَ مِن دُونِ اِ۬للَّهِ مَا لَا يَمْلِكُ لَكُمْ
ضَرّاٗ وَلَا نَفْعاٗۖ وَاللَّهُ هُوَ اَ۬لسَّمِيعُ اُ۬لْعَلِيمُۖ ﴿78﴾
قُلْ يَٰٓأَهْلَ اَ۬لْكِتَٰبِ لَا تَغْلُواْ فِے دِينِكُمْ غَيْرَ اَ۬لْحَقِّۖ
وَلَا تَتَّبِعُوٓاْ أَهْوَآءَ قَوْمٖ قَدْ ضَلُّواْ مِن قَبْلُ وَأَضَلُّواْ
كَثِيراٗ وَضَلُّواْ عَن سَوَآءِ اِ۬لسَّبِيلِۖ ﴿79﴾ لُعِنَ اَ۬لذِينَ
كَفَرُواْ مِنۢ بَنِےٓ إِسْرَٰٓءِيلَ عَلَيٰ لِسَانِ دَاوُۥدَ وَعِيسَي
اِ۪بْنِ مَرْيَمَۖ ذَٰلِكَ بِمَا عَصَواْ وَّكَانُواْ يَعْتَدُونَۖ ﴿80﴾
كَانُواْ لَا يَتَنَٰهَوْنَ عَن مُّنكَرٖ فَعَلُوهُۖ لَبِئْسَ مَا كَانُواْ يَفْعَلُونَۖ ﴿81﴾
تَرَيٰ كَثِيراٗ مِّنْهُمْ يَتَوَلَّوْنَ اَ۬لذِينَ كَفَرُواْ لَبِئْسَ مَا قَدَّمَتْ
لَهُمُۥٓ أَنفُسُهُمُۥٓ أَن سَخِطَ اَ۬للَّهُ عَلَيْهِمْ وَفِے اِ۬لْعَذَابِ هُمْ خَٰلِدُونَۖ ﴿82﴾
وَلَوْ كَانُواْ يُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ وَالنَّبِےٓءِ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيْهِ
مَا اَ۪تَّخَذُوهُمُۥٓ أَوْلِيَآءَۖ وَلَٰكِنَّ كَثِيراٗ مِّنْهُمْ فَٰسِقُونَۖ ﴿83﴾

77. Annabi Isa Dan Maryamu bai kasance ba face manzo ne, da manzanni suka fice gabansa, mahaifiyarsa kuwa mai yawan bada gaskiyace, sun kasance suna cin abinci, ka dubaka ga ƙaƙa muke bayanin ayoyi garesu, sannan ka dubaka gani ƙaƙa suke bijirewa ga buran ban gaskiya?

(WANI ABU DAGA MIYAGUN HALAYEN AHALUL KITABI)

78. Cene (dasu) "Donme kuke bautawa wanin Allah, abinda bazai mallaki cuta ko amfani a gareku ba, Ubangiji shine mai ji masani (da haluluwanku)".
79. Cene, "Ya mazowa Littafi kada kuyi shisshigi cikin addininku sai gaskiya, kadaku ,bi soye -soyen zukatan mutane da suka ɓata tun gaba, suka ɓatar da yawaici daga mutane, suka ɓace ga buran hanya madaidaiciya.
80. An tsinewa waɗanda suka kafirta na daga Bani-Isra'ila a kan harshen Annabi Dawuda (Alai-hissalamu, yai mugun yar addu'a agaresu aka mayar da su burrai, sune mutanan Ailata,) da harshen Isa Dan Maryamu (Alaihissalamu, yayi musu mugunyar addu'a aka mayar dasu alhinzirai, sune ma'abota , ɓaki). Wancanenka tsinewa, saboda sun saɓi Allah da kasancewarsu masu shisshigi.
81. Sun kasance basa hana juna ga buran aikin munkari da suka aikata shi, Lallai tur! da abinda suka kasance suna aikatawa.
82. Kana ganin yawaici daga gare-su, suna jiɓintar waɗanda suka kafirta (mutanen Makka don ƙiyayyagareka,) haƙiƙa abinda kawukansu ta gabatar garesu ya mugusta, Allah yayi fushi a garesu, su madauwama ne a cikin azaba.
83. Dasun kasance sun bada gaskiya da Allah da Annabi (Sallallahu alaihi wasallama,) da abinda aka saukar izuwa gareshi, da bazasu riƙe su ababan daukaka ba, sai dai yawaici daga garesu fasiƙai ne.

(YAHUDU DA NASARA DA ALKARSU DA MUMINAI)

* لَتَجِدَنَّ أَشَدَّ ٱلنَّاسِ عَدَٰوَةً لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱلْيَهُودَ وَٱلَّذِينَ أَشْرَكُواْۖ
وَلَتَجِدَنَّ أَقْرَبَهُم مَّوَدَّةً لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّا نَصَٰرَىٰۚ
ذَٰلِكَ بِأَنَّ مِنْهُمْ قِسِّيسِينَ وَرُهْبَانًا وَأَنَّهُمْ لَا يَسْتَكْبِرُونَ ﴿84﴾
وَإِذَا سَمِعُواْ مَآ أُنزِلَ إِلَى ٱلرَّسُولِ تَرَىٰٓ أَعْيُنَهُمْ تَفِيضُ مِنَ ٱلدَّمْعِ
مِمَّا عَرَفُواْ مِنَ ٱلْحَقِّۖ يَقُولُونَ رَبَّنَآ ءَامَنَّا فَٱكْتُبْنَا مَعَ ٱلشَّٰهِدِينَ ﴿85﴾
وَمَا لَنَا لَا نُؤْمِنُ بِٱللَّهِ وَمَا جَآءَنَا مِنَ ٱلْحَقِّ وَنَطْمَعُ أَن يُدْخِلَنَا رَبُّنَا
مَعَ ٱلْقَوْمِ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿86﴾ فَأَثَٰبَهُمُ ٱللَّهُ بِمَا قَالُواْ جَنَّٰتٍ تَجْرِي مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ
خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ وَذَٰلِكَ جَزَآءُ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿87﴾ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَآ
أُوْلَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَحِيمِ ﴿88﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تُحَرِّمُواْ طَيِّبَٰتِ مَآ أَحَلَّ ٱللَّهُ
لَكُمْ وَلَا تَعْتَدُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلْمُعْتَدِينَ ﴿89﴾ وَكُلُواْ مِمَّا رَزَقَكُمُ ٱللَّهُ حَلَٰلًا
طَيِّبًاۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ ٱلَّذِيٓ أَنتُم بِهِۦ مُؤْمِنُونَ ﴿90﴾ لَا يُؤَاخِذُكُمُ ٱللَّهُ بِٱللَّغْوِ
فِيٓ أَيْمَٰنِكُمْ وَلَٰكِن يُؤَاخِذُكُم بِمَا عَقَّدتُّمُ ٱلْأَيْمَٰنَۖ فَكَفَّٰرَتُهُۥٓ إِطْعَامُ عَشَرَةِ
مَسَٰكِينَ مِنْ أَوْسَطِ مَا تُطْعِمُونَ أَهْلِيكُمْ أَوْ كِسْوَتُهُمْ أَوْ تَحْرِيرُ رَقَبَةٍۖ
فَمَن لَّمْ يَجِدْ فَصِيَامُ ثَلَٰثَةِ أَيَّامٍۚ ذَٰلِكَ كَفَّٰرَةُ أَيْمَٰنِكُمْ إِذَا حَلَفْتُمْۚ
وَٱحْفَظُوٓاْ أَيْمَٰنَكُمْۚ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمْ ءَايَٰتِهِۦ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿91﴾

حزب

84. (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama) Lallai zaka sami mafi tsananin mutane ƙiyayyaga waɗanda suka bada gakiya Yahudu da mushirikan Makka. (saboda nunkuwar kafircinsu da jahilcinsu da son zuciyarsu,) kuma Lallai zaka sami mafi kusancinsu soyayyaga waɗanda suka bada gaskiya (Waɗanda sukace mu Nasara ne ai kusancin soyayyar wancananka (su ga muminai saboda akwai malamai daga garesu da masu ibada, kuma cewa su haƙiƙa basa girman kai (ga buran bin gaskiya tamfar girman kan Yahudu da mushirikan Makka. Ta sauka ne a cikin ƙungiyar Najashi da sukazo daga Habasha, Manzon Allah ya karanta musu Suratu Yasin sukayi kuka suka Musulunta sukace wannan ya kamanci abinda yake sauka ga Annabi Isa ƙwarai).

85. Idan sun ji abinda aka saukar bisa manzo (na alƙur'ani,) kana ganin idanuwansu tana kwararar hawaye saboda abinda suka sani na daga gaskiya, suna cewa "Ya Ubangijinmu, mun gaskata (AnnabinKa da Littafinka,) rubutamu tareda waɗanda suka shaida (da wannan)".

86. (Suka faɗa don amsa ga wanda ya Laifanta su da Musulunci na daga Yahudawa) 'Saboda mene bazamu bada gaskiya da Allah ba, da abinda yazo mana na daga gaskiya (alƙur'ani) mu yi ƙaunar cewa Ubangijinmu ya shigar da mu aljanna tareda mutane salihai?.

87. Sai Ubangiji ya saka musu aljannatai saboda wannan magana tasu, wadda ƙoramai ke kwarara ƙarƙashinta, masu dauwama a cikinta. Wancananka sakamakon masu kyautatawa aiki ke nan.

88. Waɗanda suka kafirta suka ƙaryatada ayoyinmu, waɗancananka sune "yan wuta.

TSANANTAWA DA FAIFAYEWA A CIKIN ADDINI

(Yayin da waɗansu Sahabbai suka himmatu a kan su Lazumci azimi da ƙiyamillaili da rashin kusantar matada turare da rashin cin nama da rashin yin bacci a kan shimfida, sai Allah yace);

89. Yaku waɗanda suka bada gaskiya kadaku ,haramta daɗaɗan abinda Allah ya halatta muku, kada kuyi shisshigi, Ubangiji ba yason masu shisshigi.

90. Kuci daga daɗaɗan abinda Allah ya halatta muku halal daddada, kuji tsoron Allah wandaku ,kuka bada gaskiya dashi.

(RANTSE - RANTSE DA KAFFARARTA)

91. Allah baya riƙon kuda tuntuɓen harshe a cikin rantse -rantsenku sai dai yana riƙonkune a bisa abinda kuka ƙudire rantse -rantse a kansa, kuka rantse da niyya, to, kaffara tasa ci da miskini goma, mudu ga kowane miskini, daga matsakaicin abinda kuke ci da iyalanku, ko tufatar dasu riga da rawani da gyauto, ko "yanta wuyayen mumina, to, wanda bai sami ɗaya daga abinda aka ambata ba, to, saiya azumci kwana uku, wancananka abin ambato kaffaran rantse - rantsenku ke nan. Idan kun rantse kuma kukayi kari, ku kiyaye rantse rantsenku kadaku ,warware ta, muddan bata kasance bisa aikin gyaran alheri tsakanin mutane ba. Tamfar da aka bayyana muku abinda aka faɗa yake bayyana muku ayoyinsa gareku don ku gode masa.

ثمن

* يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّمَا ٱلْخَمْرُ وَٱلْمَيْسِرُ وَٱلْأَنصَابُ وَٱلْأَزْلَٰمُ
رِجْسٌ مِّنْ عَمَلِ ٱلشَّيْطَٰنِ فَٱجْتَنِبُوهُ لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿92﴾
إِنَّمَا يُرِيدُ ٱلشَّيْطَٰنُ أَن يُوقِعَ بَيْنَكُمُ ٱلْعَدَٰوَةَ وَٱلْبَغْضَآءَ فِي ٱلْخَمْرِ
وَٱلْمَيْسِرِ وَيَصُدَّكُمْ عَن ذِكْرِ ٱللَّهِ وَعَنِ ٱلصَّلَوٰةِ فَهَلْ أَنتُم مُّنتَهُونَ ﴿93﴾
وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ وَٱحْذَرُواْ فَإِن تَوَلَّيْتُمْ فَٱعْلَمُوٓاْ
أَنَّمَا عَلَىٰ رَسُولِنَا ٱلْبَلَٰغُ ٱلْمُبِينُ ﴿94﴾ لَيْسَ عَلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ
ٱلصَّٰلِحَٰتِ جُنَاحٌ فِيمَا طَعِمُوٓاْ إِذَا مَا ٱتَّقَواْ وَّءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
ثُمَّ ٱتَّقَواْ وَّءَامَنُواْ ثُمَّ ٱتَّقَواْ وَّأَحْسَنُواْ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿95﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَيَبْلُوَنَّكُمُ ٱللَّهُ بِشَيْءٍ مِّنَ ٱلصَّيْدِ تَنَالُهُۥٓ أَيْدِيكُمْ
وَرِمَاحُكُمْ لِيَعْلَمَ ٱللَّهُ مَن يَخَافُهُۥ بِٱلْغَيْبِ فَمَنِ ٱعْتَدَىٰ بَعْدَ ذَٰلِكَ
فَلَهُۥ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿96﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَقْتُلُواْ ٱلصَّيْدَ وَأَنتُمْ حُرُمٌ
وَمَن قَتَلَهُۥ مِنكُم مُّتَعَمِّدًا فَجَزَآءٌ مِّثْلُ مَا قَتَلَ مِنَ ٱلنَّعَمِ يَحْكُمُ بِهِۦ
ذَوَا عَدْلٍ مِّنكُمْ هَدْيًۢا بَٰلِغَ ٱلْكَعْبَةِ أَوْ كَفَّٰرَةُ طَعَامِ مَسَٰكِينَ أَوْ عَدْلُ ذَٰلِكَ
صِيَامًا لِّيَذُوقَ وَبَالَ أَمْرِهِۦ عَفَا ٱللَّهُ عَمَّا سَلَفَ وَمَنْ عَادَ
فَيَنتَقِمُ ٱللَّهُ مِنْهُ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ ذُو ٱنتِقَامٍ ﴿97﴾

(GIYA DA CACA DA HADARINSU)

92. Yaku wađanda suka bada gaskiya, to, giya dai da caca da gumaka da kyamare dauđa ce daga aikin shaidan, ku nesance ta don ku rabauta,
93. Shi shaiđan dai yana nufin ya afkar da adawa ne da gaba tsakaninku a cikin giya da caca, Yakuma tsare ku ga buran ambaton Allah da kuma sallah. To, shin ku bazaku hanu bane ga buran aikata su?
94. Kubi Allah kubi manzonsa (Sallallahu alaihi wasallama,) kuji tsoron saɓonni. To, idan kuka bada bayaga buran đa'a, to, ku sani iyadda aike mabayyanine kađai a kan manzanmu.

(MARTABOBIN MUSULUNCI GUDA UKU WACCE ITACE ADDINI)

95. Ba Laifi ga wađanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagari a cikin abinda suka đanđana (na giya da caca gaban haramci,) idan sukaji tsoron (maharumul - Lahi,) suka bada gaskiya sukayi aiki nagari a maƙamin Musulunci, sannan sukaji tsoron Allah suka bada gaskiya a maƙanin imani, sannan sukaji tsoron Allah suka kyautata aiki a maƙamin ihsani Allah yana son masu kyakkyawan aiki.

(FARAUTA CIKIN IHRAMI DA SAKAMAKONTA)

96. Ya wađanda suka bada gaskiya Lallai Ubangiji yana jarrabakuda aiko muku wani abin na fa-rauta, wanda hannayenku take kama kananansa, masunku suke samun manyansa, (wannan ya auku a Hudaibiya, alhali su sun yi harama da Umra an đaiđaita kisan Sayyadina Usmanu, Annabi Sallallahu alaihi wasallama yayi mubaya'a ƙarƙashin itaciya sai namun daji da tsuntsaye suka dinga zuwa musu har gida) saboda Allah ya nuna wanda yake tsoronsa a take, to, wanda yayi shisshigi bayan wancananka hani, to, azaba mai rađađi na gareshi.
97. Ya wađanda suka bada gaskiya, ka daku ,kashe farauta alhali kuna cikin harama da hajji ko umra, wanda ya kashe daga cikin kuda gangan to; sakamakonsa na kansa, shine kwatanci na daga abinda ya kashe na daga dabba, mutum biyu ma'abuta adalci daga gareku za suyi hukunci dashi hadaya dazai isa Ka'aba (a yanka shi a Harami ayi sadaka dashi bisa miskinan harami ko kuwa) kaffara Itace ci da miskinan, ko misalin wannan ciyarwa na azumi, (ya azumce shi rana kowane mudu,) saboda ya đanđani kuđar Lamarinsa. Allah yayi rangwame ga abinda ya wuce (na kisan farauta gaban haramtawa,) wanda yakoma (izuwa gareshi kuwa) Allah zai masa azaba, Allah mabuwayi ne mai azaba (ga wanda ya saɓe shi).

أُحِلَّ لَكُمْ صَيْدُ الْبَحْرِ وَطَعَامُهُۥ مَتَاعًا لَّكُمْ وَلِلسَّيَّارَةِ
وَحُرِّمَ عَلَيْكُمْ صَيْدُ الْبَرِّ مَا دُمْتُمْ حُرُمًا وَاتَّقُوا اللَّهَ
الَّذِي إِلَيْهِ تُحْشَرُونَ ﴿96﴾ * جَعَلَ اللَّهُ الْكَعْبَةَ الْبَيْتَ الْحَرَامَ
قِيَامًا لِّلنَّاسِ وَالشَّهْرَ الْحَرَامَ وَالْهَدْيَ وَالْقَلَائِدَ
ذَٰلِكَ لِتَعْلَمُوا أَنَّ اللَّهَ يَعْلَمُ مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ
وَأَنَّ اللَّهَ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمٌ ﴿97﴾ اعْلَمُوا أَنَّ اللَّهَ شَدِيدُ الْعِقَابِ
وَأَنَّ اللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿98﴾ مَّا عَلَى الرَّسُولِ إِلَّا الْبَلَاغُ
وَاللَّهُ يَعْلَمُ مَا تُبْدُونَ وَمَا تَكْتُمُونَ ﴿99﴾ قُل لَّا يَسْتَوِي الْخَبِيثُ
وَالطَّيِّبُ وَلَوْ أَعْجَبَكَ كَثْرَةُ الْخَبِيثِ فَاتَّقُوا اللَّهَ
يَا أُولِي الْأَلْبَابِ لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿100﴾ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا
لَا تَسْأَلُوا عَنْ أَشْيَاءَ إِن تُبْدَ لَكُمْ تَسُؤْكُمْ وَإِن تَسْأَلُوا عَنْهَا حِينَ
يُنَزَّلُ الْقُرْآنُ تُبْدَ لَكُمْ عَفَا اللَّهُ عَنْهَا وَاللَّهُ غَفُورٌ حَلِيمٌ ﴿101﴾
قَدْ سَأَلَهَا قَوْمٌ مِّن قَبْلِكُمْ ثُمَّ أَصْبَحُوا بِهَا كَافِرِينَ ﴿102﴾ مَا جَعَلَ اللَّهُ
مِن بَحِيرَةٍ وَلَا سَائِبَةٍ وَلَا وَصِيلَةٍ وَلَا حَامٍ وَلَٰكِنَّ الَّذِينَ كَفَرُوا
يَفْتَرُونَ عَلَى اللَّهِ الْكَذِبَ وَأَكْثَرُهُمْ لَا يَعْقِلُونَ ﴿103﴾

98. An halatta muku farautar kogi (kuna masu harama da hajji ko kuwa ba masu harama dashi ba, shine abinda baya (ayuwa sai a cikin kogi kamar kifi) abincin kogi (wanda ya jefo shi a mace) don jiyarwar dađi gareku, da matafiya (daga gareku suyi guzurinsa,) an haramta muku farautar sarari, (shine abinda yake rayuwa a cikin sarari na daga namun daji, kadaku ,farauce shi) muddin kuna saye da harami, ku tsoraci Allah wanda izuwa gareshi ake taraku.

(DAKIN ALLAH MAI ALFARMA DA WATA MAI ALFARMA)

99. Allah yasanya Ka'aba đaki mai alfarma rayuwa ga mutane, al'amarin addininsu na hajji yake tsayawa saboda shi, da lamarin duniyarsu, da wata mai alfarma (wato watanni masu alfarma, Zulƙa'ada, Zulhajji, Muharram, Rajab saboda amincewar yaƙi a cikinsu, da hadaya da rataye ratayenta, saboda Mai su ya amince ba mai kamasu Wancananka don ku sani Allah yasan duk abinda yake sammai da ƙassai. Haƙiƙa Ubangiji masanine shi da komai (saboda sanyawarsa wannan don jawo masalahohi gareku, da ije cuce -cuce ga buranku tun kafin aukuwarta, dalili ne cewa Allah yasan duk abinda yake cikin sammai da ƙassaida abindazai kasance harabada).

(KWADAITARWA DA TSORATARWA)

100. Ku sani haƙiƙa Allah mai tsan-anin uƙubane (ga maƙiyansa,) kuma Allah mai yawan gafara ne (ga masoyansa) kuma mai jinƙai (garesu).

101. Ba wani abu a kan Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) sai ida aike. Allah yasan abinda kuke ɓoyewa da bayyanawa.

102. Cene (dasu) "haram da halal bazai daidai ba, koda yawan haramiyar nan ya baka ƙaye kuji tsoron Allah (a cikin barinsa) ya ma'abuta hankula don ku ra-bauta.

(TAMBAYA MAI CUTARWA WATO TA'ANNUTI)

(Ta sauka ne yayin da suka yawaita tambayar Annabi Sallallahu alaihi wasallama).

103. Yaku wanđada suka bada gaskiya, kar kuyi tambayo ga abubuwa in an bayyana muku ta baƙanta muku, in kun tambayo gareta zamanin da ake saukar da ƙur' ani (zamanin Annabi SallAllahu alaihi wasallama) a bayyana muku ita, (wato idan kun yi tambayo ga abubuwa a zamaninsa alƙur'ani saiya sauka da bayyana muku ita, kodayaushe kuma ya bayyanata saiya baƙanta muku, to, saboda haka kada kuyi tanibayo a kanta). Allah yayi muku afuwa ga buran tambayo da kuka yi, (to kadaku ,kuma,) Allah mai gafara ne maijinkirin azaba.

104. Haƙiƙa mutanen dasuke gabanku, sun tambayi (Annabawansu) ita, akayi musu bayanin hukunce - hukuncenta, sannan suka zama masu kafircewa da ita (da rashin aiki da ita).

(WANJ ABU DAGA SHA' ANIN JAHILIYYA)

105. Allah bai shar'anta nonon gunki[1] ba, wala bayansa[2], wala uwarta mata[3], wala uban maza[4], sai dai wađanda suka kafirta suna ƙin ƙiran karya bisa Allah, yawaicinsu basu da hankali.

(YIN AIKI DA DOKAR ALƘUR'ANI)

1) Nonon gunki· "Bahira" Wanda baza'a sha non-on ta ba, sabodata gunki ce.
2) Bayansa: "Sa'ibatin" bayan gunki, wato baza'a dora masa kaya ba.
3) Uwar mata: "Wasilatin" Waccc ta fara haihuwa da tanata ta biyantada tamata.
4) Uban maza: "Hami" Wanda akai baye dashi da yawa kamar goma ko tara.

وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ تَعَالَوْاْ إِلَىٰ مَا أَنزَلَ اللَّهُ وَإِلَى الرَّسُولِ
قَالُواْ حَسْبُنَا مَا وَجَدْنَا عَلَيْهِ ءَابَآءَنَا أَوَلَوْ كَانَ ءَابَآؤُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ
شَيْـٔاً وَلَا يَهْتَدُونَ ﴿106﴾ يَٰٓأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُواْ عَلَيْكُمُۥٓ أَنفُسَكُمْ
لَا يَضُرُّكُم مَّن ضَلَّ إِذَا اهْتَدَيْتُمُۥٓ إِلَى اللَّهِ مَرْجِعُكُمْ جَمِيعاً
فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿107﴾ * يَٰٓأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُواْ شَهَادَةُ ثمن
بَيْنِكُمُۥٓ إِذَا حَضَرَ أَحَدَكُمُ الْمَوْتُ حِينَ الْوَصِيَّةِ اثْنَانِ ذَوَا عَدْلٍ
مِّنكُمْ أَوْ ءَاخَرَانِ مِنْ غَيْرِكُمُۥٓ إِنْ أَنتُمْ ضَرَبْتُمْ فِي الْأَرْضِ
فَأَصَابَتْكُم مُّصِيبَةُ الْمَوْتِ تَحْبِسُونَهُمَا مِنۢ بَعْدِ الصَّلَوٰةِ فَيُقْسِمَانِ
بِاللَّهِ إِنِ ارْتَبْتُمْ لَا نَشْتَرِي بِهِۦ ثَمَناً وَلَوْ كَانَ ذَا قُرْبَىٰ
وَلَا نَكْتُمُ شَهَادَةَ اللَّهِ إِنَّا إِذاً لَّمِنَ الْاثِمِينَ ﴿108﴾ فَإِنْ عُثِرَ عَلَىٰٓ
أَنَّهُمَا اسْتَحَقَّآ إِثْماً فَـَٔاخَرَانِ يَقُومَانِ مَقَامَهُمَا مِنَ الَّذِينَ اسْتُحِقَّ
عَلَيْهِمُ الْأَوْلَيَانِ فَيُقْسِمَانِ بِاللَّهِ لَشَهَادَتُنَا أَحَقُّ مِن شَهَادَتِهِمَا وَمَا اعْتَدَيْنَا
إِنَّا إِذاً لَّمِنَ الظَّٰلِمِينَ ﴿109﴾ ذَٰلِكَ أَدْنَىٰ أَن يَأْتُواْ بِالشَّهَادَةِ
عَلَىٰ وَجْهِهَا أَوْ يَخَافُواْ أَن تُرَدَّ أَيْمَانُۢ بَعْدَ أَيْمَانِهِمْ وَاتَّقُواْ
اللَّهَ وَاسْمَعُواْ وَاللَّهُ لَا يَهْدِي الْقَوْمَ الْفَٰسِقِينَ ﴿110﴾

106. Idan Ance dasu kuzo izuwa abinda Allah ya saukar, kuzo izuwa hukuncin Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama na halacci da haramci,) saisu ce;abinda muka sami iyayenmu kai na addini da shari'a ya ishe mu, (wađannan mutane basu da bambanci da mutanen zamanin nan namu, da suka sa dokar kafirci a gaba, suka fifita ta a kan Alƙur'ani da shari'ar Annabi Sallallahu alaihi wasallama. Sai Ubangiji yace,) "Yanzu wannan ya ishe su, ko da iyayensu basu san komai ba, basa kuma shiriya (izuwa gaskiya?)"

(UMARNI GA AIKIN DA'A DA HANI GA AIKIN MUNKARI)

107. Ya wađanda suka bada gaskiya! ku kula da kanku (da babbadayaro ikowa yai ta kansa) wanda ya ɓata bazai cuce ku ba in kun shiriya. Makomarku ta tabbata izuwa Allah dakiđaya, ya Labarta muku abinda kuka kasance kuna aikatawa.

(SHAHADA A KAN WASIYYA YAYIN MUTUWA DA HUKUNCINTA)

108. Ya wađanda suka bada gaskiya, shaidar tsakaninku idan sabubban mutuwa suka halarci dayan ku, zamanin wasiyya,mutum biyu ma'abuta adalci daga cikin ku (Musulmi) ko kuwa wađansu biyun daga wanin addininku in ku kun yi tafiya a cikin ƙasa musibar mutuwa ta Sameku wato Mutawa, ku tsaishe su bayan sallar (La'asar) su rantse da Allah in kun yi kokwanto a cikin shaidar, (wato sigar mntsuwar) Barna musanyo tamani maimakon Allah a kan ƙarya ba, (wato koda abin rantsewar nan saboda shiya ka-sance ma'abucin zumunci ne namu, bazamu ɓoye shaidar Allah ba,) hakika mu yayin nan muna cikin masu zunibi.

109. Idan akayi tsinkaye (bayan rantsuwarsu) a kan cewa su Lallai sun cancani Laifi, (ha'inci ko ƙarya a cikin shaida) to, wađansu biyu đin su tsaya matsayinsu na da ga wađanda sukafi kusa da mataccen, aka cancanta wasiyya a kansu, (wato suna magada) su rantse da Allah (a bisa ha'incin shaidun,) haƙiƙa shaidarmu tafi gaskiya daga shaidarsu, bamu yi shisshigi a cikin rantsuwa ba, mu, haƙiƙa yayin nan Lallai muna cikin azzalumai.

110. Wannan (hukunci abin ambato na maida rantsuwa kan magada) shine yafi kusa izuwa shaidun nan su zoda shaida a kan yadda take, ko mafi kusa izuwa suji tsoron a maida rantse - rantse bayan rantse rantsensu (a kan magada masu da'awa su rantse kan ha'incinsu su kunyata, su rama abu,) kuji tsoron Allah, kuji (abinda ake umarninku dashi). Allah baya shiriyar mutane fasiƙai.

(ALƘIYAMA!!!)

يَوْمَ يَجْمَعُ ٱللَّهُ ٱلرُّسُلَ فَيَقُولُ مَاذَآ أُجِبْتُمْ قَالُواْ لَا عِلْمَ لَنَآ
إِنَّكَ أَنتَ عَلَّٰمُ ٱلْغُيُوبِ ﴿١١١﴾ إِذْ قَالَ ٱللَّهُ يَٰعِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ
ٱذْكُرْ نِعْمَتِي عَلَيْكَ وَعَلَىٰ وَٰلِدَتِكَ إِذْ أَيَّدتُّكَ بِرُوحِ ٱلْقُدُسِ
تُكَلِّمُ ٱلنَّاسَ فِي ٱلْمَهْدِ وَكَهْلًا وَإِذْ عَلَّمْتُكَ ٱلْكِتَٰبَ
وَٱلْحِكْمَةَ وَٱلتَّوْرَىٰةَ وَٱلْإِنجِيلَ وَإِذْ تَخْلُقُ مِنَ ٱلطِّينِ
كَهَيْـَٔةِ ٱلطَّيْرِ بِإِذْنِي فَتَنفُخُ فِيهَا فَتَكُونُ طَيْرًا بِإِذْنِي
وَتُبْرِئُ ٱلْأَكْمَهَ وَٱلْأَبْرَصَ بِإِذْنِي وَإِذْ تُخْرِجُ ٱلْمَوْتَىٰ
بِإِذْنِي وَإِذْ كَفَفْتُ بَنِي إِسْرَٰٓءِيلَ عَنكَ إِذْ جِئْتَهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ
فَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنْهُمْ إِنْ هَٰذَآ إِلَّا سِحْرٌ مُّبِينٌ ﴿١١٢﴾
۞ وَإِذْ أَوْحَيْتُ إِلَى ٱلْحَوَارِيِّـۧنَ أَنْ ءَامِنُواْ بِي وَبِرَسُولِي
قَالُوٓاْ ءَامَنَّا وَٱشْهَدْ بِأَنَّنَا مُسْلِمُونَ ﴿١١٣﴾ إِذْ قَالَ ٱلْحَوَارِيُّونَ
يَٰعِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ هَلْ يَسْتَطِيعُ رَبُّكَ أَن يُنَزِّلَ عَلَيْنَا
مَآئِدَةً مِّنَ ٱلسَّمَآءِ قَالَ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿١١٤﴾
قَالُواْ نُرِيدُ أَن نَّأْكُلَ مِنْهَا وَتَطْمَئِنَّ قُلُوبُنَا وَنَعْلَمَ
أَن قَدْ صَدَقْتَنَا وَنَكُونَ عَلَيْهَا مِنَ ٱلشَّٰهِدِينَ ﴿١١٥﴾

ربع

111. Ambaci ranar da Allah yake tara manzanni ranar Alƙiyama, yace (dasu) "Me aka amsa 340 muku? (dashi zamanin da kukayi kira izuwa kaɗaita Allah (tau-hidi) "Sukacc ba sani garemu ga wannan, haƙiƙa kaine masanin asirin fake". (Zasu faɗi haka saboda firgitada zata tafi da iliminsu sannan su shaidar a kan al'uinmansu a yayin da suka nutsu).

(MU'UJIZOZIN ANNABI ISA ALAIHISSALAMU)

112. ka ambata zamanin da Allah yake faɗa ga Annabi Isa (Alaihissalamu) "Tuna ni'imata gareka da mahaifiyarka, (wato gode min,) zamanin dana ƙarfafe ka da ran tsarki (Jibrila Alaihissalamu,) kana zantar da mutane a cikin gunya da kuma kana gwarzo, (an fahinci saukarsa gaban alƙiyama saboda an ɗauke shine gaban gwarzantaka tamkar da aka faɗa a cikin Suratu Ali Imrana) da kuma zamanin dana sanar dakai mbutu da ilimi mai amfani da Attaura da Linjila da zamanin da kake halittar kamar surar tsuntsu daga taɓo, da izinina, kai busa a cikinta ta zama tsuntsu da izinina (wato nufina,) kake warkar da makaho da kuturu da izinina, kake fitar da matattu daga ƙaburburansu suna rayayyu da izinina dayayin dana kame Bani - Isra'ila ga buran ka (Lokacin da sukayi nufin kashe ka) yayin dakazo musu da mu'ujizozi, sai waɗanda suka kafirta daga cikinsu Sukace,"Wannan abinda ka zo dashi bai kasance ba sai tsafi mabayyani".

113. Da zamanin dana aiko izuwa Hawariyawa (a bisa harshensa,) Ku bada gaskiya dani da manzona (Annabi Isa,) Sukace, "Mun bada gaskiya (dasu,) shaida da cewa mu, haƙiƙa Musulmi ne".

(ƘISSAR MA'IDATI 'KA BAKI")

114. Kuma ka ambata yayin da Hawariyawa Sukace, "Ya Annabi Isa yanzu kuwa Ubangijinka zai iya saukar mana da kaɓaki daga sama?" Sai (Annabi Isa) yace (dasu) "Kuji tsoron Allah, (a cikin kago waɗannan ayoyi) in kun kasance muminai".

115. Sukace, "Muna nufi ne da wannan roƙo namu don mu ci daga gareta, zuciyarmu ta nutsu da ƙarin yakini mu tabbatacewa kayi mana gaskiya (cikin da'awar Annabci) mu kasance daga masu shaidawa a kanta".

(FARANCE - FARANCEN CIKI NA MAULIDODI NA ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA DANA WALIYYAI)

قال عيسى ابن مريم اللهم ربنا أنزل علينا مائدة من السماء
تكون لنا عيدا لأولنا وءاخرنا وءاية منك وارزقنا وأنت
خير الرازقين ﴿116﴾ قال الله إني منزلها عليكم فمن يكفر بعد منكم
فإني أعذبه عذابا لا أعذبه أحدا من العالمين ﴿117﴾ وإذ قال الله
يا عيسى ابن مريم ءأنت قلت للناس اتخذوني وأمي إلهين من دون
الله قال سبحانك ما يكون لي أن أقول ما ليس لي بحق إن كنت
قلته فقد علمته تعلم ما في نفسي ولا أعلم ما في نفسك
إنك أنت علام الغيوب ﴿118﴾ ما قلت لهم إلا ما أمرتني به
أن اعبدوا الله ربي وربكم وكنت عليهم شهيدا ما دمت فيهم
فلما توفيتني كنت أنت الرقيب عليهم وأنت على كل شيء شهيد ﴿119﴾
إن تعذبهم فإنهم عبادك وإن تغفر لهم فإنك أنت العزيز الحكيم ﴿120﴾
قال الله هذا يوم ينفع الصادقين صدقهم لهم جنات
تجري من تحتها الأنهار خالدين فيها أبدا رضي الله
عنهم ورضوا عنه ذلك الفوز العظيم ﴿121﴾ لله ملك
السماوات والأرض وما فيهن وهو على كل شيء قدير ﴿122﴾

116. Annabi Isa Dan Maryama (Alaihissalamu) yace, "Ya ma'abucin sufofi kyawawa dasunaye madaukaka, ya Ubangijinmu saukar da kabaki a garemu, ranar saukar sa, ya zama idi a garemu, (mu girmama shi) ga na farkon mu dana ƙarshen mu, da (wandazaizo bayan mu,) ya zama aya daga gareka (da annabcina,) ka azurta mu da ita, kaine fiyayyen masu azurta wa"

117. Sai Ubangiji yace, (Yana mai amsawa gareshi,) "Haƙiƙa ni zan saukar da ita a gareku, wanda ya kafirta bayan saukar ta, to, haƙiƙa ni zan yi masa azaba, azabar da bazan azabci wani daga talikai irin ta ba". (Sai Mala'iku suka sauko da ita daga sama, akwai, gurasa akanta guda bakwai, da kifi bakwai suka ci daga gareta har suka ƙoshi).

(KUBUTAR DA ANNABI ISA DAGA ABINDA NASARA SUKAYI DA'AWA A KANSA)

118. Ka ambata zamanin da Ubangiji yace (da Annabi Isa ranar alƙiyama don kurustawa ga mutanensa, yace): "Ya Isa Dan Maryamu yanzu kaine kace da mutane ku riƙe ni da uwata ubangiji guda biyu ba Allah ba? "Annabi Isa yace (alhali yana makyarkyata); "Tsarki ya tabbata a gareka (ga buran abinda bai dace dakai bana sharika da waninsa,) bazai yiwu gare ni bana faɗi abinda bani da gaskiya a cikinsa, in na faɗi wannan magana haƙiƙa ka sani, kasan abinda na ɓoye a cikin raina, ban san abinda ka ɓoye a cikin Zatinka ba, haƙiƙa kai Kaine mas-anin asirin fake".

119. "Ban gaya musu komai basa abinda ka umarce ni dashi, sh ne ku bautawa Allah Ubangijim Ubangijinku, ni na kasance ma shaida a garesu muddan ina gurinsu to amma, a yayin daka dauke ni izuwa gareka, kaine ka zama mai kulawa a kansu, kai mai ganine mai tsinkaye a kan komai.

120. In kai musu azaba to su bayinka ne (sai yadda kayi dasu ba mai cewa donme,) in kayi gafara garesu, (wato ga wanda ya bada gaskiya daga cikinsu) to, haƙiƙa kaine mabuwayi gwani.

121. Ubangiji yace, "Wannan ranar alƙiyama rana ce da gaskiya take amfanin masu gaskiya (kamar Annabi Isa Alaihissalamu gama ranar sakamako ce,) aljannatai na garesu, wacce ƙoramu take gudana ƙarƙashinta, masu dauwama a cikin ta har abada, Allah yayi yarda garesu, (da da'arsa,) sun yarda da Allah (da sakamakonsa,) Wannan shine rabo mai girma.

122. Mulkin sammai da ƙassaina Ubangiji ne (taskokin ruwa , tsiri, arziki da wanin wannan) da abinda yake cikinsu, shi mai iko ne a bisa komai.

6 سُورَةُ الأَنْعَامِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ مِائَةٌ وَسَبْعٌ وَسِتُّونَ آيَةً 167

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

ثمن

* الْحَمْدُ لِلَّهِ الَّذِي خَلَقَ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضَ وَجَعَلَ الظُّلُمَٰتِ
وَالنُّورَ ① ثُمَّ الَّذِينَ كَفَرُوا بِرَبِّهِمْ يَعْدِلُونَ ② هُوَ الَّذِي خَلَقَكُم
مِّن طِينٍ ثُمَّ قَضَىٰ أَجَلًا وَأَجَلٌ مُّسَمًّى عِندَهُ ثُمَّ أَنتُمْ تَمْتَرُونَ ③
وَهُوَ اللَّهُ فِي السَّمَٰوَٰتِ وَفِي الْأَرْضِ يَعْلَمُ سِرَّكُمْ وَجَهْرَكُمْ وَيَعْلَمُ مَا تَكْسِبُونَ ④
وَمَا تَأْتِيهِم مِّنْ ءَايَةٍ مِّنْ ءَايَٰتِ رَبِّهِمْ إِلَّا كَانُوا عَنْهَا مُعْرِضِينَ ⑤
فَقَدْ كَذَّبُوا بِالْحَقِّ لَمَّا جَاءَهُمْ فَسَوْفَ يَأْتِيهِمْ أَنۢبَٰٓؤُا مَا كَانُوا بِهِ
يَسْتَهْزِءُونَ ⑥ أَلَمْ يَرَوْا كَمْ أَهْلَكْنَا مِن قَبْلِهِم مِّن قَرْنٍ مَّكَّنَّٰهُمْ
فِي الْأَرْضِ مَا لَمْ نُمَكِّن لَّكُمْ وَأَرْسَلْنَا السَّمَاءَ عَلَيْهِم مِّدْرَارًا وَجَعَلْنَا
الْأَنْهَٰرَ تَجْرِي مِن تَحْتِهِمْ فَأَهْلَكْنَٰهُم بِذُنُوبِهِمْ وَأَنشَأْنَا مِنۢ بَعْدِهِمْ
قَرْنًا ءَاخَرِينَ ⑦ وَلَوْ نَزَّلْنَا عَلَيْكَ كِتَٰبًا فِي قِرْطَاسٍ فَلَمَسُوهُ بِأَيْدِيهِمْ
لَقَالَ الَّذِينَ كَفَرُوا إِنْ هَٰذَا إِلَّا سِحْرٌ مُّبِينٌ ⑧ وَقَالُوا لَوْلَا أُنزِلَ عَلَيْهِ
مَلَكٌ وَلَوْ أَنزَلْنَا مَلَكًا لَّقُضِيَ الْأَمْرُ ثُمَّ لَا يُنظَرُونَ ⑨

SURATUL AN'AMI

A Makka Aka Saukar Da Ita wato gaban hijira Ayoyinta Dari Da Sittin Da bakwai (167)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabaɗaya, mai jinƙan Muminai A Lahira a keɓe

(DALILAN WAHADANIYYA DA TASHIN ALƘIYAMA DA GAMAWAR ILIMIN UBANGIJI)

1. Godiya ta tabbata ga Ubangiji wanda ya halicci sammai da ƙassai, ya halicci duffai da haske.
2. Sannan waɗanda suka kafirta suna daidaita wanin Ubangiji da Ubangiji a cikin bauta.
3. Shine wanda ya halicce.ku daga yunɓu (da halittar ubanku Annabi Adamu dagashi) sannan yasanya muku ajali abin ambato nan gareshi (zaku mutu a ƙarshensa) sannan ku kuna kokwanto (a cikin tashin alƙiyama).
4. Shine Allah a cikin sammai da ƙassai, yasan asirinkuda bayyananku, sannan yasan abinda kuke aikatawa (na hairi ko sharri).

(SABABIN KAFIRCINSU DA AƘIBARSA)

5. Wani abu bazai zowa mutanen Makka daga ayoyin Ubangijinsu ba, face sun kasance masu bujirewa ga buransa.
6. Haƙiƙa sun ƙaryatada gaskiya (Alƙur'ani yayin dayazo musu,) da sannu sakamakon abinda suke izgili dashi zaizo musu.
7. Ba sayi duba ba (a cikin tafiye-tafiyensu zuwa ƙasashen Sham,) nawa muka halakar daga gabansu na daga tsaraikuda muka tabbatar dasu a ƙasa, (da karfi dayalwatar arziki, abinda bamu makkanan muku ba, muka sako, ruwa daga sama mai kwarara a garesu muka sanya ƙoramu mai kwarara ƙarƙashinsu, muka halakar dasu saboda zunubansu, muka fari waɗansu al'ummar daban bayansu.

(SHUBUHOHINSU A CIKIN AIKE DA RADDI KANTA)

8. Da mun saukar da Littafi a gareka a cikin takarda tamfar da suka nema suka shafa shi da hannuwansu, da waɗanda suka kafirta sunce, "Wannan bai ka-sance ba sai tsafi mabayyani".
9. Saisu ce, "Donme ba a saukar da Mala'ika a gareshi bashi Annabi sallallahu alaihi wasallama?" Da mun saukar da Mala'ika a (kamar yadda suka nema,) da sai a hukunta al'amari da halakarsu, sannan baza a saurara musu donsu tuba ba.

وَلَوْ جَعَلْنَٰهُ مَلَكاً لَّجَعَلْنَٰهُ رَجُلاً وَلَلَبَسْنَا عَلَيْهِم مَّا يَلْبِسُونَ ﴿10﴾
وَلَقَدُ اُسْتُهْزِئَ بِرُسُلٍ مِّن قَبْلِكَ فَحَاقَ بِالذِينَ سَخِرُواْ
مِنْهُم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿11﴾ قُلْ سِيرُواْ فِي الْأَرْضِ
ثُمَّ اُنظُرُواْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ الْمُكَذِّبِينَ ﴿12﴾ قُل لِّمَن
مَّا فِي السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ قُل لِّلَّهِ كَتَبَ عَلَىٰ نَفْسِهِ الرَّحْمَةَ
لَيَجْمَعَنَّكُمْ إِلَىٰ يَوْمِ الْقِيَٰمَةِ لَا رَيْبَ فِيهِ الذِينَ خَسِرُواْ
أَنفُسَهُمْ فَهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿13﴾ * وَلَهُۥ مَا سَكَنَ فِي الَّيْلِ وَالنَّهَارِ
وَهُوَ السَّمِيعُ الْعَلِيمُ ﴿14﴾ قُلْ أَغَيْرَ اللَّهِ أَتَّخِذُ وَلِيّاً فَاطِرِ السَّمَٰوَٰتِ
وَالْأَرْضِ وَهُوَ يُطْعِمُ وَلَا يُطْعَمُ قُلْ إِنِّيَ أُمِرْتُ أَنْ أَكُونَ
أَوَّلَ مَنْ أَسْلَمَ وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ الْمُشْرِكِينَ ﴿15﴾
قُلْ إِنِّيَ أَخَافُ إِنْ عَصَيْتُ رَبِّيَ عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿16﴾
مَن يُصْرَفْ عَنْهُ يَوْمَئِذٍ فَقَدْ رَحِمَهُۥ وَذَٰلِكَ الْفَوْزُ
الْمُبِينُ ﴿17﴾ وَإِن يَمْسَسْكَ اللَّهُ بِضُرٍّ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥ إِلَّا هُوَ
وَإِن يَمْسَسْكَ بِخَيْرٍ فَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ﴿18﴾
وَهُوَ الْقَاهِرُ فَوْقَ عِبَادِهِۦ وَهُوَ الْحَكِيمُ الْخَبِيرُ ﴿19﴾

ربع

10. Da mun sanyashi Mala'ika da mun maidashi mutum (donsu iyaganinsa,) da kuma mun cuɗanyagaresu abinda suke rikitarwa a kan kansu, (shine su ce, "Wannan bai kasance ba sai mutum kamar kai)".

(RARRASHIN ANNABI SALLALAHU ALAIHI WASALLAMA)

11. Haƙiƙa an yi izgili da manzanni gabanka, abinda suke izgili n dashiya sauka ga waɗanda suke izgili n nan daga cikinsu,
12. Cene (dasu) "Kuyi tafiya a bayan ƙasa sannan ku duba yaya ƙarshen masu ƙaryatawa da mazanni ta kasance, (an halakar dasu da azaba).

(TABBATAR DA WAHADINIYYA DA TASHIN ALƘiYAMA)

13. Cene (dasu) "Abinda yake cikin sammai da ƙassaina waye?" Cene "Na Allah ne" (in basu amsa ba) Allah ya wajabta raha-ma akan kansa don falala daga gareshi (wannan tausasawa ne izuwa kira ga Allah) Lallai zai tara ku a cikin ranar alƙiyama don yayi muku sakamako, babu kokwanto a cikinsa, waɗanda suka taɓar da kawunansu, su bazasu bada gaskiya ba.
14. Duk abinda ya tabbata cikin dare da rana na Ubangiji ne, shine mai ji mai gani.
15. Cene (dasu) "Yanzu wanin Allah zan riƙa abin bautawa, mahaliccin sammai da ƙassai, shine mai azurta wa ba a azurta shi," (kai! baza tayiwu ba,) Cene (dasu) "Ni an umarce ni na kasance farkon wanda ya miƙa wuyaga Allah (daga wannan al'umma,") (Ance da ni) karka kasance daga cikin mushirikai da Allah.
16. Cene (dasu) haƙiƙa ni ina jin tsoron azabar rana maigirma, in na saɓi Ubangijina.
17 Wanda aka juyar dashi ga buransa a wannan rana, haƙiƙa Allah yajiƙansa, Wancananka shine rabo mabayyani.

DOGARO GA ALLAH

18. In Ubangiji ya same ka da bala'i (kamar rashin Lafiyako talauci,) to, ba mai yaye maka sai shi, in ya same ka da alheri (kamar Lafiya da wadata,) to, shi mai iko ne bisa komai.
19. Shine mai rinjaye birbishin bayinsa, shine gwani cikin halitta tasa, mai cikakken sani da zahirinsu da baɗininsu.

(GAMAWAR KIRAN ANNABI 5ALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA HAR ZUWA RANAR ALKIYAWA)

A yayin da sukace da Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama zo mana da abinda zamu shaida gareka da Annabci, saboda mazowa Littafi suna musun ka, sai Allah yace.

قُلْ أَيُّ شَيْءٍ أَكْبَرُ شَهَادَةً قُلِ اللَّهُ شَهِيدٌ بَيْنِي وَبَيْنَكُمْ وَأُوحِيَ إِلَيَّ
هَٰذَا الْقُرْآنُ لِأُنذِرَكُم بِهِ وَمَن بَلَغَ أَئِنَّكُمْ لَتَشْهَدُونَ أَنَّ مَعَ اللَّهِ
آلِهَةً أُخْرَىٰ قُل لَّا أَشْهَدُ قُلْ إِنَّمَا هُوَ إِلَٰهٌ وَاحِدٌ وَإِنَّنِي بَرِيءٌ مِّمَّا
تُشْرِكُونَ ﴿20﴾ الَّذِينَ آتَيْنَاهُمُ الْكِتَابَ يَعْرِفُونَهُ كَمَا يَعْرِفُونَ أَبْنَاءَهُمُ
الَّذِينَ خَسِرُوا أَنفُسَهُمْ فَهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿21﴾ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ افْتَرَىٰ
عَلَى اللَّهِ كَذِبًا أَوْ كَذَّبَ بِآيَاتِهِ إِنَّهُ لَا يُفْلِحُ الظَّالِمُونَ ﴿22﴾ وَيَوْمَ نَحْشُرُهُمْ
جَمِيعًا ثُمَّ نَقُولُ لِلَّذِينَ أَشْرَكُوا أَيْنَ شُرَكَاؤُكُمُ الَّذِينَ كُنتُمْ
تَزْعُمُونَ ﴿23﴾ ثُمَّ لَمْ تَكُن فِتْنَتُهُمْ إِلَّا أَن قَالُوا وَاللَّهِ رَبِّنَا
مَا كُنَّا مُشْرِكِينَ ﴿24﴾ انظُرْ كَيْفَ كَذَبُوا عَلَىٰ أَنفُسِهِمْ وَضَلَّ عَنْهُم
مَّا كَانُوا يَفْتَرُونَ ﴿25﴾ * وَمِنْهُم مَّن يَسْتَمِعُ إِلَيْكَ وَجَعَلْنَا عَلَىٰ ثمن
قُلُوبِهِمْ أَكِنَّةً أَن يَفْقَهُوهُ وَفِي آذَانِهِمْ وَقْرًا وَإِن يَرَوْا كُلَّ آيَةٍ
لَّا يُؤْمِنُوا بِهَا حَتَّىٰ إِذَا جَاءُوكَ يُجَادِلُونَكَ يَقُولُ الَّذِينَ كَفَرُوا إِنْ هَٰذَا
إِلَّا أَسَاطِيرُ الْأَوَّلِينَ ﴿26﴾ وَهُمْ يَنْهَوْنَ عَنْهُ وَيَنْأَوْنَ عَنْهُ وَإِن يُهْلِكُونَ
إِلَّا أَنفُسَهُمْ وَمَا يَشْعُرُونَ ﴿27﴾ وَلَوْ تَرَىٰ إِذْ وُقِفُوا عَلَى النَّارِ فَقَالُوا
يَا لَيْتَنَا نُرَدُّ وَلَا نُكَذِّبَ بِآيَاتِ رَبِّنَا وَنَكُونَ مِنَ الْمُؤْمِنِينَ ﴿28﴾

20. Cene (dasu) "Wane abu ne mafi girman shaida?" Cene (dasu) tsakanina da ku"Allah ne shaida (a bisa gaskiyata,) an aiko wannan Alƙur'ani izuwa gareni, domin (in tsoratar daku ,dashi,) Yaku mutanen Makka da wanda Alƙur'an ya riska (na mutum da aljan har izuwa ranar alƙiyama). Yanzu ku kwa shaida cewa akwai iyayen giji tareda Allah?" Cene (dasu) "Ni bazan shaida da haka ba," Cene, "Haƙiƙa shi Allah abin bautawa ne gudaɗaya kawai, haƙiƙa ni makubuci ne daga abinda kuke tarawa (na abin bautawa tareda Allah)".

KAMAN NIN ANNABI S.A.W) A CIKIN LIT TAT TAFAN DA SUKA GABATA IZUWA YAU DA BASU DANNU BA.

21. Waɗanda muka basu Littafi, sunsanshi (Annabi Sallallahu alaihi wasallama a cikin Littafinsu,) tamfar da sukasan 'ya'yansu- Waɗanda suka taɓar da kawukansu (daga garesu,) su bazasu bada gakiyaba (wato waɗanda Allah yasan taɓewarsu tun azal).
22. To, ba mafi zalunci daga wanda ya ƙirƙiri ƙarya bisa Ubangiji, (da dangana shariki gareshi,) ko ya ƙaryata ayoyinsa (Alƙur'ani,) haƙiƙa al'amarin azzalumai bazasu tsira ba.
23. Ka ambaci ranar da muke tara su bakiɗaya, sannan mu faɗa ga waɗanda sukayi shirka (don umstawa, wato woho) "Ina iyayen gijin nakuda kuke riyawa (cewa su sharikaine ga Allah?)".
24. To, sannan ba wani abu daya zama hanzarinsu, face cewarsu "Wallahi Allah bamu kasance mushurikai ba."
25. Duba (Ya Muhammadu Sallallahu alaika wasallama) ƙaƙa sukayi ƙarya a kan kawukansu, abinda suke ƙirƙirar sa ga Allah ya bace musu.

(SASHIN AIKACE - AIKACEN MUSHURIKAI)

26. Akwai daga garesu wanda yake sauraro izuwa gareka (idan kana karatu,) mun sanya rufe - rufe a kan zukatansu don kadasu fahimci al'ƙur'ani, mun sanya kumnta a cikin kunnuwansu, in sun ga kowace aya bazasu bada gaskiya da ita ba har idan sun zo maka suna jayayya da kai. Waɗanda suka kafirta suna cewa; "Wannan alƙur'ani bai kasance ba illa ƙaryace ƙaryacen mutanen farko".
27. Su suna hana mutane bin Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) suna nisanta ga buransa, (basa bada gaskiya dashi,) basa halakarwa sai kansu, amma basa hasashen (wannan).

(MATSAYIN KAFIRAI A RANAR ALƘIYAMA)

28. Da kana duba (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama) zamanin da aka bujirar dasu kan wuta, suka ce; kai! da ma a koma da mu (duniya) mu zamo bazamu ƙaryatada ayoyin ubangijinmu ba, mu kasance daga muminai, (daka ga al'amari maigirma)".

بل بدا لهم ما كانوا يخفون من قبل ولو ردوا لعادوا لما نهوا عنه
وإنهم لكاذبون ﴿29﴾ وقالوا إن هي إلا حياتنا الدنيا وما نحن
بمبعوثين ﴿30﴾ ولو ترى إذ وقفوا على ربهم قال أليس هذا بالحق
قالوا بلى وربنا قال فذوقوا العذاب بما كنتم تكفرون ﴿31﴾
قد خسر الذين كذبوا بلقاء الله حتى إذا جاءتهم الساعة
بغتة قالوا يا حسرتنا على ما فرطنا فيها وهم يحملون
أوزارهم على ظهورهم ألا ساء ما يزرون ﴿32﴾ وما الحياة
الدنيا إلا لعب ولهو وللدار الآخرة خير للذين يتقون
أفلا تعقلون ﴿33﴾ قد نعلم إنه ليحزنك الذي يقولون فإنهم
لا يكذبونك ولكن الظالمين بآيات الله يجحدون ﴿34﴾ ولقد
كذبت رسل من قبلك فصبروا على ما كذبوا وأوذوا حتى
أتاهم نصرنا ولا مبدل لكلمات الله ولقد جاءك من نبإ
المرسلين ﴿35﴾ وإن كان كبر عليك إعراضهم فإن استطعت
أن تبتغي نفقا في الأرض أو سلما في السماء فتأتيهم بآية
ولو شاء الله لجمعهم على الهدى فلا تكونن من الجاهلين ﴿36﴾

29. Haba! abinda suka kasancesuna ƃoyewa ne tun gabaya bayyana garesu, (shine faɗinsu Wallahi Allah mu bamu kasance mushirikai bada shaidawar gabubuwansu sukayi dana shina a kan wannan) da an koma dasu duniya din ma (taƙadiran) dasun koma ga abinda aka hane su ga buransa (na daga shirka,) haƙiƙa su maƙaryata ne, (a cikin alƙawarin imani).

30. Sukace (su masu musun tashin alƙiyama) "Ba wata rayuwa sai rayuwarmu ta duniya, mu ba ababen tasa ne ba".

(WANI ABU DAGA MATSAYIN KAFIRAI A RANAR ALƘIYAMA HAR YAU)

31. Da kana gani zamanin da aka bujirar dasu ga Ubangijinsu, (daka ga al'amari maigirma,) Yace (dasu bisa harshen Mala'iku don woho) "Yanzu wannan tashin ba gaskiyaba ne?" Sukace "Gaskiya ne mana, Wallahi," (Allah) yace to, "Ku ɗanɗani azaba saboda kun kasance kuna kafircewa".

32. Waɗanda sukayi musun saduwa da Allah da tashin alƙiyama, haƙiƙa sun taɓe, har sai sanda alƙiyama tazo musu bazato, su ce "Ya kaitonmu! a bisa sakacinmu a duniya, su suna ɗauke da zunubansu a kan bayayyakinsu, (zatazo musu ranar tashin alƙiyama a cikin mafi munin halitta, mafi ɗoyi ta haye kansu, to jama'a, tir da wannan kaya nasu dasuke ɗauke dashi!.

33. Rayuwar duniyabata kasance ba sai wasa da shagala (ga buran aikin ɗa'a,) Lallai Lahira iTace tafi ga masu jin tsoron Allah. Shin ba kwayi hankali bane ku saduda.

(RARRASHIN ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA DA AL'ADAR ALLAH A CIKIN HALITTARSA)

34. Haƙiƙa mun sani cewa sha'anin abinda suke faɗa (na ƙaryata ka) yana baƙanta maka rai, haƙiƙa su, basa dangana ka izuwa ƙarya (Don sun , san magasgaci ne kai,) kai dai azzalumai suna musun ayoyin Allah ne.

35. Haƙiƙa an rasa gasgata Annabawa gaban ka (akwai rairashi ga ma'aiki a cikin wannan magana). Sai suka daure a kan abinda a kai musu na karyatawa, an cuce su, har taimakonmu yazo musu, (to kai ma ka daure har taimako yazo maka da halakar da mutanen ka,) ba mai musanyawa ga alƙawarin Ubangiji, haƙiƙa daga Labarin manzanni yazo maka abindazai nitsar da zuciyarka.

36. Idan bujirewarsu ta girmama gareka, (saboda kwaɗayinka a kan shinyansu,) to, idan kana da iko ka gina gidan ƙasa ko tsani a cikin sama kazo musu da aya (daga abinda suka shato, to, sai ka yi! wato baka da iko a kan wannan sai ka daure har Allah yayi hukuncinsa,) da Allah yaga damar shiriyarsu daya tara su a kan shiriya, to, kadaka zamo daga cikin jahilai (da wannan).

حزب

* إِنَّمَا يَسْتَجِيبُ الَّذِينَ يَسْمَعُونَ وَالْمَوْتَىٰ يَبْعَثُهُمُ اللَّهُ ثُمَّ إِلَيْهِ
يُرْجَعُونَ ﴿37﴾ وَقَالُوا لَوْلَا نُزِّلَ عَلَيْهِ ءَايَةٌ مِّن رَّبِّهِ قُلْ إِنَّ اللَّهَ
قَادِرٌ عَلَىٰ أَن يُنَزِّلَ ءَايَةً وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿38﴾
وَمَا مِن دَابَّةٍ فِي الْأَرْضِ وَلَا طَائِرٍ يَطِيرُ بِجَنَاحَيْهِ إِلَّا أُمَمٌ
أَمْثَالُكُم مَّا فَرَّطْنَا فِي الْكِتَابِ مِن شَيْءٍ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّهِمْ يُحْشَرُونَ ﴿39﴾
وَالَّذِينَ كَذَّبُوا بِآيَاتِنَا صُمٌّ وَبُكْمٌ فِي الظُّلُمَاتِ مَن يَشَإِ
اللَّهُ يُضْلِلْهُ وَمَن يَشَأْ يَجْعَلْهُ عَلَىٰ صِرَاطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿40﴾
قُلْ أَرَأَيْتَكُمْ إِنْ أَتَاكُمْ عَذَابُ اللَّهِ أَوْ أَتَتْكُمُ السَّاعَةُ أَغَيْرَ اللَّهِ
تَدْعُونَ إِن كُنتُمْ صَادِقِينَ ﴿41﴾ بَلْ إِيَّاهُ تَدْعُونَ فَيَكْشِفُ
مَا تَدْعُونَ إِلَيْهِ إِن شَاءَ وَتَنسَوْنَ مَا تُشْرِكُونَ ﴿42﴾ وَلَقَدْ
أَرْسَلْنَا إِلَىٰ أُمَمٍ مِّن قَبْلِكَ فَأَخَذْنَاهُم بِالْبَأْسَاءِ وَالضَّرَّاءِ
لَعَلَّهُمْ يَتَضَرَّعُونَ ﴿43﴾ فَلَوْلَا إِذْ جَاءَهُم بَأْسُنَا تَضَرَّعُوا
وَلَٰكِن قَسَتْ قُلُوبُهُمْ وَزَيَّنَ لَهُمُ الشَّيْطَانُ مَا كَانُوا يَعْمَلُونَ ﴿44﴾
فَلَمَّا نَسُوا مَا ذُكِّرُوا بِهِ فَتَحْنَا عَلَيْهِمْ أَبْوَابَ كُلِّ شَيْءٍ
حَتَّىٰ إِذَا فَرِحُوا بِمَا أُوتُوا أَخَذْنَاهُم بَغْتَةً فَإِذَا هُم مُّبْلِسُونَ ﴿45﴾

(WANI ABU DAGA TAURIN KAN MUSHIRIKAI)

37. Waɗanda suke jin Alƙur'ani jin fahimta su kaɗai ne suke ansawa kiran ka izuwa imani, kafirai kuwa waɗanda aka kwatantada matattu a cikin rashin ji, Allah zai tashe su (a Lahira,) sannan izuwa gareshi za a koma dasu.

38. Kafiran Makka suka ce; "Donme ba a saukar da aya daga Ubangijinsa a gareshi bakamar taguwa da saukar da kaɓaki?" Cene (dasu) Ubangiji mai iko ne a bisa ya saukar da aya (daga abinda suka shato) sai dai yawaicinsu basu san (cewa saukar ta bala'i ne a kansu ba, saboda wajabcin halakarsu in sun musunta).

DO GARO GA ALLAH

39 Babu daga wata dabbada take tafiya daga cikin kasa, wala tsuntsu da yake tashi a hawa da fukafukansa, face al'ummai ne kamar ku, (a cikin shirya halittar tada arzikintada halayanta,) Bamu yi sakacin wani abu ba a cikin Lauhul Mahfuzi komai ƙanƙantarsa ya zama bamu rubuta shi ba, sannan izuwa Ubangijinsu za a tara su (yayi hukunci tsakaninsu, yayi sakayya da balama daga mai kaho, sannan yace dasu ku zama turɓaya).

40. Waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu (Alƙur'ani,) kurame ne (ga buran jin ta jin ƙarba,) bebaye ne (ga buran fadin gaskiya, suna cikin duffan kafirci,) Wanda Allah yaso ɓatar dashi saiya ba-tar dashi, wanda yaso shiriya tasa saiya sanyashi a kan tafarki madaidaici (Dinil Isalami).

(IZUWA ALLAH BAYI SUKE FAKEWA A CIKIN TSANANCE TSANANCE TAREDA MUSALCE -MUSALCE DA AL'UMMAR DATA WUCE)

41. Gaya musu "Ku bamu Labari, in azabar Allah tazo muku, aduniyako kuwa alƙiyama tazo muku bagtatan,yanzu wanin Allah zaku kira, (a'a!) In kun ka-sance masu gaskiya (a cikin cewa gumaka zata amfane ku, to, ku kira ta").

42. Kai! Shi kaɗai zaku kira (a cikin tsanance - tsanance,) ya yaye.muku abinda kuke kiransa izuwa gareku na tsanani inyaga damar yayewar, kuna mance abinda kuke shirkantawa tare dashi (na gumaka, bazaku kirawo su ba).

43. Haƙiƙa mun aiko manzanni izuwa al'ummai, daga gabanka, (suka ƙaryata su, sai) muka kama su da tsananin talauci da rashin Lafiya,donsu ƙanƙanda - kai a garemu su saduda.

44. To, mai ya hana, zamanin da az-abarmu tazo musu, su ƙanƙanda - kai sai dai zukatansu ta ƙeƙashe ne, shaiɗan ya ƙawata musu abinda suke aikatawa na saɓo.

45. To, yayin da suka mance abinda aka gargaɗar dasu dashi (na daga tsanani da rashin Lafiya, basu wa'azantu ba,) sai muka buɗe musu ƙofofin kowane abu (na ni'i'momi don maƙarƙashiya a garesu,) har Lokacin da idan sukayi farim. cikin abinda aka basu, (farin cikin girmań kai);sai mukazo musu da azaba bagtatan, sai gasu masu ɗebewar haso daga dukkan alheri.

فَقُطِعَ دَابِرُ الْقَوْمِ الَّذِينَ ظَلَمُواْ وَالْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ الْعَٰلَمِينَ ﴿46﴾
قُلْ أَرَآيْتُمُۥ إِنْ أَخَذَ اللَّهُ سَمْعَكُمْ وَأَبْصَٰرَكُمْ وَخَتَمَ عَلَىٰ قُلُوبِكُم
مَّنْ إِلَٰهٌ غَيْرُ اللَّهِ يَأْتِيكُم بِهِ انظُرْ كَيْفَ نُصَرِّفُ الْآيَٰتِ ثُمَّ هُمْ
يَصْدِفُونَ ﴿47﴾ قُلْ أَرَآيْتَكُمُۥ إِنْ أَتَىٰكُمْ عَذَابُ اللَّهِ بَغْتَةً أَوْ جَهْرَةً
هَلْ يُهْلَكُ إِلَّا الْقَوْمُ الظَّٰلِمُونَ ﴿48﴾ وَمَا نُرْسِلُ الْمُرْسَلِينَ
إِلَّا مُبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ فَمَنْ ءَامَنَ وَأَصْلَحَ فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ
وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿49﴾ وَالَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يَمَسُّهُمُ
الْعَذَابُ بِمَا كَانُواْ يَفْسُقُونَ ﴿50﴾ * قُل لَّا أَقُولُ لَكُمْ
عِندِے خَزَآئِنُ اللَّهِ وَلَا أَعْلَمُ الْغَيْبَ وَلَا أَقُولُ لَكُمْ إِنِّے مَلَكٌ
إِنْ أَتَّبِعُ إِلَّا مَا يُوحَىٰ إِلَيَّ قُلْ هَلْ يَسْتَوِے الْأَعْمَىٰ وَالْبَصِيرُ
أَفَلَا تَتَفَكَّرُونَ ﴿51﴾ وَأَنذِرْ بِهِ الَّذِينَ يَخَافُونَ أَن يُحْشَرُواْ
إِلَىٰ رَبِّهِمْ لَيْسَ لَهُم مِّن دُونِهِ وَلِيٌّ وَلَا شَفِيعٌ لَّعَلَّهُمْ
يَتَّقُونَ ﴿52﴾ وَلَا تَطْرُدِ الَّذِينَ يَدْعُونَ رَبَّهُم بِالْغَدَوٰةِ وَالْعَشِيِّ
يُرِيدُونَ وَجْهَهُۥ مَا عَلَيْكَ مِنْ حِسَابِهِم مِّن شَےْءٍ وَمَا مِنْ حِسَابِكَ
عَلَيْهِم مِّن شَےْءٍ فَتَطْرُدَهُمْ فَتَكُونَ مِنَ الظَّٰلِمِينَ ﴿53﴾

ثمن

46. Sai aka tunbuke asalin mutanen da sukayi zalunci. Godiya ta tabbata ga Ubangijin talikai (a kan nasarar manzanni da halakar da kafirai).

(WANI ABU NA DALILAN TAUHIDI HAR YAU)

47. Gaya musu "Ku bani Labari, in Ubangiji ya riƙe kunnuwanku (kuka kurumce,) da gannanku, (kuka makance,) ya yimƙe bisa zukatanku, (baku san komai ba,) Wane Ubangiji ne ba Allah bazaizo muku dashi?" Duba ƙaƙa muke bayanin ayoyi a kan wahadaniyarmu, sannan su suke bujirewa (ga buranta basa bada gaskiya).
48. Cene (dasu) "Ku bamu Labari in azabar Ubangiji tazo muku bagtatan ko ƙarara (da dare ko da rana,) ba a halakar da kowa sai mutane azzalumai.
49. Barna aiko manzanni face masu albishir ga wanda ya bada gaskiya (da aljanna,) masu gargaɗin wanda ya kafirta (da wuta,) to, wanda ya bada gaskiya (dasu,) ya kyautata aikinsa to, ba tsoro a garesu, su baza suyi baƙin ciki ba (a Lahira).
50. waɗanda suka karyatada ayoyinmu azabazata shafe su saboda kasancewarsu suna fasikanci, (suna kangara ga da'ar Allah).

(MUHIMMAN ABUBUWA GURIN MANZANNI DA NAUYIN MANZANTAKA)

51. Cene dasu, Ni bana cewa (da ku) "Taskokin Allah na gareni (wacce yake azurta bayi daga gareta,)" kuma bana cewa "Na san gaibu, "kuma bana cewa (da ku) "Ni Mala'ika ne," Ni bana bin komai sai abinda aka saukar izuwa gareni. Cene "yanzu kafiri da mumini sayi daidai?" (a'a!) Donme ba kwa tunani ku bada gaskiya.
52. Ka tsoratar da waɗanda suke tsoron a tara su zuwa Ubangijinsu da alƙur'ani, basu da wani majiɓinci bashi ba, wala mai ceto, donsuji tsoron Allah.

(WAZIFOFIN SHAIHUNNAI DA HIZIBANSU DA HALARORINSU NA SAFIYA DAYAMMACI) HAR YAU .

53. Karka kore waɗanda suke bau-tawa Ubangijinsu safiya dayammaci, suna nufin Zatin Allah (da ibadarsu, ba wani abu na daga tarkacen duniya ba, sune fuƙara'u, mushirikai sun yi suka cikinsu, sun nufi yakore su donya zauna dasu, Annabi kuwa tsiran Allah da amincinsa ya tabbata a gareshi dai yayi nufin wannan don kwaɗayi a cikin Musuluncinsu,) ba wani abu na Lissafinsu a kanka ba wani abu na Lissafin ka a kansu, bare ka kore su ka zamo daga cikin az-zalumai.

وَكَذَٰلِكَ فَتَنَّا بَعْضَهُم بِبَعْضٍ لِّيَقُولُوٓاْ أَهَٰٓؤُلَآءِ مَنَّ ٱللَّهُ عَلَيْهِم
مِّنۢ بَيْنِنَآ أَلَيْسَ ٱللَّهُ بِأَعْلَمَ بِٱلشَّٰكِرِينَ ﴿54﴾ وَإِذَا جَآءَكَ
ٱلَّذِينَ يُؤْمِنُونَ بِـَٔايَٰتِنَا فَقُلْ سَلَٰمٌ عَلَيْكُمْ كَتَبَ رَبُّكُمْ
عَلَىٰ نَفْسِهِ ٱلرَّحْمَةَ أَنَّهُۥ مَنْ عَمِلَ مِنكُمْ سُوٓءَۢا بِجَهَٰلَةٍ
ثُمَّ تَابَ مِنۢ بَعْدِهِۦ وَأَصْلَحَ فَإِنَّهُۥ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿55﴾ وَكَذَٰلِكَ
نُفَصِّلُ ٱلْأٓيَٰتِ وَلِتَسْتَبِينَ سَبِيلَ ٱلْمُجْرِمِينَ ﴿56﴾ قُلْ إِنِّي
نُهِيتُ أَنْ أَعْبُدَ ٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ
قُل لَّآ أَتَّبِعُ أَهْوَآءَكُمْ قَدْ ضَلَلْتُ إِذًا وَمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلْمُهْتَدِينَ ﴿57﴾
قُلْ إِنِّي عَلَىٰ بَيِّنَةٍ مِّن رَّبِّي وَكَذَّبْتُم بِهِۦ مَا عِندِي مَا تَسْتَعْجِلُونَ بِهِۦٓ
إِنِ ٱلْحُكْمُ إِلَّا لِلَّهِ يَقُصُّ ٱلْحَقَّ وَهُوَ خَيْرُ ٱلْفَٰصِلِينَ ﴿58﴾
قُل لَّوْ أَنَّ عِندِي مَا تَسْتَعْجِلُونَ بِهِۦ لَقُضِيَ ٱلْأَمْرُ
بَيْنِي وَبَيْنَكُمْ وَٱللَّهُ أَعْلَمُ بِٱلظَّٰلِمِينَ ﴿59﴾ ۞ وَعِندَهُۥ مَفَاتِحُ ربع
ٱلْغَيْبِ لَا يَعْلَمُهَآ إِلَّا هُوَ وَيَعْلَمُ مَا فِي ٱلْبَرِّ وَٱلْبَحْرِ
وَمَا تَسْقُطُ مِن وَرَقَةٍ إِلَّا يَعْلَمُهَا وَلَا حَبَّةٍ فِي ظُلُمَٰتِ
ٱلْأَرْضِ وَلَا رَطْبٍ وَلَا يَابِسٍ إِلَّا فِي كِتَٰبٍ مُّبِينٍ ﴿60﴾

54. Hakana muka janabi ba'alinsu da ba'ali, (wato manyan mutane da wulakantacce da mawadaci da talaka,) donsu manyan mutanen nan da mawadatan nan su ce, "Yanzu wadannan fukara'un sune wadanda Allah yayi musu baiwa tsakaninmu, (Sai Ubangiji yace,) "Allah masanine da masu godiyagareshi".

(WANI ABU NA DAGA RAHAMAR AKLLAH DA HALITTA)

55. Idan wadanda suka bada gaskiya da ayoyinmu sukazo maka, Cene "Gaisuwata ta tabbata gareku, Ubangiji yayi hukunci da rahama a bisa kansa, cewa sha'anin, wanda ya aikata mummuna daga cikinku'da jahilci sannan ya tuba bayan aikinsa, ya inganta aikinsa, to, hakika Ubangiji mai gafara ne mai jinkai.

56. (Tamfar da muka bayyana maka abinda muka ambata,) tamfar haka muke rarrabe maka ayoyi (na kur'ani,) don gaskiya ta bayyana ayi aiki da ita, kuma donka ga hanyar masu Laifi.

(MATSAYIN ANNABI TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARESHI)

57. Cene "hakika ni an hane ni na bautawa abinda kuke bautawa ba Allah ba". Cene (dasu) bazan bi soye - soyen zukatan ku ba, hakika na bata yayin nan, ni ban kasance cikin masu shiriya ba".

58. Cene 'Ni hakika ina kan bayani daga Ubangijina alhali kun karyata dashi, abinda kuke gaggauto shi baya wurina, hukunci bai kasance ba sai ga Allah, Allah yana hukunta gaskiya, shine mafi mahukunta iya hukunci".

59. Cene (dasu) "Da abinda kuke nemangaggauto shi na gareni da an hukunta al'amari tsakanina daku ,(in gaggauto muku shi na huta,) Allah masanine da azzalumai".

(CIKAR ILIMIN UBANGIJI SUBHANAHU WATA'ALA)

60. Mabudan gaibu na ga Ubangiji, (taskokin gaibu da hanyoyi masu sadawa izuwa saninsa,) ba wanda yasan ta sai Al'lah, (guda biyar ce wacce take cikin fadinsa, hakika Ubangiji ilimin sa'a yana gareshi har karshe, tamfar da Buhari ya ruwaito,) Yasan abinda yake faruwa a cikin jazzai da kogi, alkaryu wadanda suke gefen kogi. Wata warka bazata sarayaba face yasan ta, wala kwaya a cikin duffan kasa, wala danye wala kekashasshe, face suna cikin Littafi mai bayyanawa (lauhul Mahfuzu).

وَهُوَ ٱلَّذِي يَتَوَفَّىٰكُم بِٱلَّيْلِ وَيَعْلَمُ مَا جَرَحْتُم بِٱلنَّهَارِ ثُمَّ
يَبْعَثُكُمْ فِيهِ لِيُقْضَىٰٓ أَجَلٞ مُّسَمّٗىۖ ثُمَّ إِلَيْهِ مَرْجِعُكُمْ ثُمَّ
يُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿61﴾ وَهُوَ ٱلْقَاهِرُ فَوْقَ عِبَادِهِۦۖ وَيُرْسِلُ
عَلَيْكُمْ حَفَظَةً حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَ أَحَدَكُمُ ٱلْمَوْتُ تَوَفَّتْهُ رُسُلُنَا وَهُمْ
لَا يُفَرِّطُونَ ﴿62﴾ ثُمَّ رُدُّوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ مَوْلَىٰهُمُ ٱلْحَقِّۚ أَلَا لَهُ ٱلْحُكْمُ
وَهُوَ أَسْرَعُ ٱلْحَٰسِبِينَ ﴿63﴾ قُلْ مَن يُنَجِّيكُم مِّن ظُلُمَٰتِ ٱلْبَرِّ
وَٱلْبَحْرِ تَدْعُونَهُۥ تَضَرُّعٗا وَخُفْيَةٗ لَّئِنْ أَنجَيْتَنَا مِنْ هَٰذِهِۦ لَنَكُونَنَّ
مِنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ﴿64﴾ قُلِ ٱللَّهُ يُنَجِّيكُم مِّنْهَا وَمِن كُلِّ كَرْبٖ
ثُمَّ أَنتُمْ تُشْرِكُونَ ﴿65﴾ قُلْ هُوَ ٱلْقَادِرُ عَلَىٰٓ أَن يَبْعَثَ عَلَيْكُمْ
عَذَابٗا مِّن فَوْقِكُمْ أَوْ مِن تَحْتِ أَرْجُلِكُمْ أَوْ يَلْبِسَكُمْ شِيَعٗا وَيُذِيقَ
بَعْضَكُم بَأْسَ بَعْضٍۗ ٱنظُرْ كَيْفَ نُصَرِّفُ ٱلْأٓيَٰتِ لَعَلَّهُمْ يَفْقَهُونَ ﴿66﴾
وَكَذَّبَ بِهِۦ قَوْمُكَ وَهُوَ ٱلْحَقُّۚ قُل لَّسْتُ عَلَيْكُم بِوَكِيلٖ
لِّكُلِّ نَبَإٖ مُّسْتَقَرّٞۚ وَسَوْفَ تَعْلَمُونَ ﴿67﴾ وَإِذَا رَأَيْتَ ٱلَّذِينَ يَخُوضُونَ
فِيٓ ءَايَٰتِنَا فَأَعْرِضْ عَنْهُمْ حَتَّىٰ يَخُوضُواْ فِي حَدِيثٍ غَيْرِهِۦۚ وَإِمَّا يُنسِيَنَّكَ
ٱلشَّيْطَٰنُ فَلَا تَقْعُدْ بَعْدَ ٱلذِّكْرَىٰ مَعَ ٱلْقَوْمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿68﴾

61. Shine wanda yake karɓɓar rankuda dare, yasan abinda kuke aikatawa da rana, sannan ya tashe ku a cikin rana (da dawo da rayukanku,) donya hukunta ajali abin ambato, (ajalin rayuwa,) sannan izuwa gareshi makomar ku (izuwa tashin alƙiyama,) sannan ya baku Labari da abinda kuka kasance kuna aikatawa (sannan yayi muku hukunci dashi).

(MALA'IKU MASUKULA DA HALITTA)

62. Shine mai rinjaye birbishin bayinsa, yana aiko Mala'iku masu kiyaye aikin bayi a kanku, har Lokacin da mutuwa ta zowa ɗayanku, sai Mala'ikunmu na karɓar rai su karɓi ransa, su basa sakaci (cikin abinda aka umarce su dashi).

63. Sannan a mayar dasu izuwa Allah mana Ilakinsu na gaskiya, (kun ji ko?) Hukunci zartacce na gareshi. shine mafi gaggawar Lissafi (zaiyi wa mutane Lis-safin a gwargwadon wuni daga kwanukan duniya, wato a cikin awa shida).

(IKON ALLAH DA JINƘANSA)

64. Cene (dasu) "Waye mai tserantar daku ,daga duffan sarari dana kogi, tsarmakatansu cikin tafiye - tafiyensu, Lokacin da) kuke kiransa a sarari da ɓoye. Wallahi in ka tserar da mu daga waɗannan (tsanance - tsanance,) Lallai zamu kasance cikin masu gode maka.

65. Cene (dasu) "Allah ne mai tserar daku ,daga gareta, kuma daga dukkan baƙin ciki, sannan ku kuna shirka dashi".

(IKON ALLAH BISA AUKAR DA AZABA BISA MASU SABO 'KAMAR BAM)

66. Cene, "Shine mai iko a bisa ya aiko da azaba a kanku daka burbushinku, (kamar duwarwatsu da tsawa da bam,) ko daga ƙarkashin ƙafafuwanku (kamar kisfewa kamar ƙaruna) ko ya cuɗanYaku daban - daban, (kamar jama'un son zuciya kamar jama'u saba'in da biyu da wasu kamarsu,) ya ɗanɗana wa sashin ku azabar sashi, (dayaƙin Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi, yayin da wannan aya ta sauka sai yace, "Wannan yafi sauƙi," yayin data gabanta ta sauka sai yace, Ina neman tsari da Zatinka inji Buhari, Muslim yace; "Na roƙi Ubangiji kada ya sanya yaƙin al'ummata tsakaninsu ya hana ni," kuma yace yayin data sauka yace "Kun jiba! haƙiƙa ita zata kasance ne tawilinta bai zo bata tukuna,) "Duba ƙaƙa muke bayyana ayoyi (masu nuna ikonmu) donsu fahinci (cewa abinda suke kai ɓatacce ne).

67. Mutanen ka sun ƙaryatada alƙur'ani shine ko gaskiya, Cene (dasu) "Ni ban kasance wakili a kanku ba (bare in saka muku, ni mai gargaɗi ne kawai, al'amarin ku yana ga Allah, wannan gaban umarni dayaƙi ne) Kowane Labari akwai Lokacin tabbatarsa, haggyala! dasannu kwa gani.

(MASU IZGILI DA ALƘUR'ANI DA SAKAMAKONSU)

68. Idan ka ga waɗanda suke kutsawa cikin ayoyinmu (suke izgili da Alƙur;ani,) to,yi nesa ga buransu, sai sun kutsa cikin wani zancen bashi ba, idan shaiɗan ya mantar dakai (ka zauna taredasu,) to, kadaka zauna bayan tunawar tareda mutane azzalumai.

ثمن

وَمَا عَلَى اَ۬لذِينَ يَتَّقُونَ مِنْ حِسَابِهِم مِّن شَےْءٖ وَلَٰكِن
ذِكْرَىٰ لَعَلَّهُمْ يَتَّقُونَۖ ﴿69﴾ * وَذَرِ اِ۬لذِينَ اَ۪تَّخَذُواْ دِينَهُمْ
لَعِباٗ وَلَهْواٗ وَغَرَّتْهُمُ اُ۬لْحَيَوٰةُ اُ۬لدُّنْيَاۖ وَذَكِّرْ بِهِۦٓ أَن
تُبْسَلَ نَفْسُۢ بِمَا كَسَبَتْ لَيْسَ لَهَا مِن دُونِ اِ۬للَّهِ
وَلِيّٞ وَلَا شَفِيعٞۖ وَإِن تَعْدِلْ كُلَّ عَدْلٖ لَّا يُوخَذْ مِنْهَآۖ أُوْلَٰٓئِكَ
اَ۬لذِينَ أُبْسِلُواْ بِمَا كَسَبُواْۖ لَهُمْ شَرَابٞ مِّنْ حَمِيمٖ وَعَذَابٌ
أَلِيمُۢ بِمَا كَانُواْ يَكْفُرُونَۖ ﴿70﴾ قُلْ أَنَدْعُواْ مِن دُونِ اِ۬للَّهِ
مَا لَا يَنفَعُنَا وَلَا يَضُرُّنَا وَنُرَدُّ عَلَىٰٓ أَعْقَابِنَا بَعْدَ إِذْ هَدَىٰنَا اَ۬للَّهُ
كَالذِے اِ۪سْتَهْوَتْهُ اُ۬لشَّيَٰطِينُ فِے اِ۬لْأَرْضِ حَيْرَانَۖ
لَهُۥٓ أَصْحَٰبٞ يَدْعُونَهُۥٓ إِلَى اَ۬لْهُدَى اَ۪يتِنَاۖ قُلْ إِنَّ هُدَى اَ۬للَّهِ
هُوَ اَ۬لْهُدَىٰۖ وَأُمِرْنَا لِنُسْلِمَ لِرَبِّ اِ۬لْعَٰلَمِينَ ﴿71﴾ وَأَنْ أَقِيمُواْ
اُ۬لصَّلَوٰةَ وَاتَّقُوهُۖ وَهُوَ اَ۬لذِے إِلَيْهِ تُحْشَرُونَۖ ﴿72﴾ وَهُوَ اَ۬لذِے
خَلَقَ اَ۬لسَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضَ بِالْحَقِّۖ وَيَوْمَ يَقُولُ كُن
فَيَكُونُۖ ﴿73﴾ قَوْلُهُ اُ۬لْحَقُّۖ وَلَهُ اُ۬لْمُلْكُۖ يَوْمَ يُنفَخُ فِے اِ۬لصُّورِۖ
عَٰلِمُ اُ۬لْغَيْبِ وَالشَّهَٰدَةِۖ وَهُوَ اَ۬لْحَكِيمُ اُ۬لْخَبِيرُۖ ﴿74﴾

69. Babu wani abu na Lissaflnsu masu Kutsawa a kan wađanda suke jin tsoron Allah, kayi gargađi garesu donsu tsoraci kutsawar.
70. Rabu da wađanda suka riƙi addininsu wasa da shagala, rayuwar duniya ta ruđe su, (wannan gaban umarni dayaƙi) ka gargađar da mutane da Alƙur;ani, don kada wata kai a miƙa ta (izuwa halaka,) da abindata aikata, batada wani mataimaki ba Allah ba, ba wani mataimaki dazai hana mata azabar Allah, in tai fansar dukkan fansa, baza a karɓi fansar nan daga gareta ba, Wađancananka, sune wađanda aka mika su ga halaka saboda abinda suka aikata, abin sha na ruwa mai tsananin zafi na garesu da azaba mai rađađi saboda kafircinsu.

(MUSULUNCI DASHIRKA)

71. Cene (dasu) yanzu ma bautawa ba Allah ba abinda bazai amfane mu da bautarsa ba, bazai cuce mu (da barinta, sune gu-maka,) a mayar da mu mushirikai a bisa digadiganmu, bayan Ubangiji ya shirye mu (izuwa Musulunci,) kamar wanda shaiđanu suka ɓatar dashi a cikin ƙasa, dimautacce yana da abokai suna kiransa izuwa shiriya (suna ce dashi) "Zo garemu, (ba amsa musu baya halaka,) to, Cene "haƙiƙa shiriyar Allah (Musulunci) shine shiriya, (waninsa ɓata ne,) an umarce mu mu miƙa wuya izuwa Ubangijin talikai".
72. An umarce ku mu tsaida sallah, kuji tsoron Ubangiji wanda ake tara ku izuwa gareshi (ranar alƙiyama don sakamako).
73. Shine wanda ya halicci sammai da ƙassaida gaskiya, ka ambaci ranar da yake cewa (da abu) "Samu" saiya samu, (shine ranar alƙiyama yace da halitta ku tashi sai ko su tashi).
74. Maganarsa ce gaskiya, wacce ba kokwanto a cikinta, mulki na gareshi ranar da ake busa a cikin ƙaho, (busa ta biyu daga Israfilu, ba wani mai mulki a wannan rana sai Allah,) Masa-nin asirin fake dana sarari, shine gwani mai cikakken sani.

(YADDA ANNABI IBRAHIM ALAIHISSALAMU YABAR SHIRKA)

وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِيمُ لِأَبِيهِ ءَازَرَ أَتَتَّخِذُ أَصْنَامًا ءَالِهَةً
إِنِّيَ أَرَىٰكَ وَقَوْمَكَ فِي ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿75﴾ وَكَذَٰلِكَ نُرِيَ
إِبْرَٰهِيمَ مَلَكُوتَ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَلِيَكُونَ مِنَ الْمُوقِنِينَ ﴿76﴾
فَلَمَّا جَنَّ عَلَيْهِ اللَّيْلُ رَءَا كَوْكَبًا قَالَ هَٰذَا رَبِّيَ
فَلَمَّا أَفَلَ قَالَ لَا أُحِبُّ الْأٓفِلِينَ ﴿77﴾ فَلَمَّا رَءَا الْقَمَرَ
بَازِغًا قَالَ هَٰذَا رَبِّيَ فَلَمَّا أَفَلَ قَالَ لَئِن لَّمْ يَهْدِنِي رَبِّي
لَأَكُونَنَّ مِنَ الْقَوْمِ الضَّآلِّينَ ﴿78﴾ فَلَمَّا رَءَا الشَّمْسَ
بَازِغَةً قَالَ هَٰذَا رَبِّي هَٰذَا أَكْبَرُ فَلَمَّا أَفَلَتْ قَالَ يَٰقَوْمِ إِنِّي
بَرِيٓءٌ مِّمَّا تُشْرِكُونَ ﴿79﴾ إِنِّي وَجَّهْتُ وَجْهِيَ لِلذِي فَطَرَ السَّمَٰوَٰتِ
وَالْأَرْضَ حَنِيفًا وَمَا أَنَا مِنَ الْمُشْرِكِينَ ﴿80﴾ ۞ وَحَآجَّهُ قَوْمُهُ ربع
قَالَ أَتُحَآجُّونِي فِي اللَّهِ وَقَدْ هَدَىٰنِ وَلَا أَخَافُ مَا تُشْرِكُونَ بِهِ
إِلَّا أَنْ يَّشَآءَ رَبِّي شَيْـًٔا وَسِعَ رَبِّي كُلَّ شَيْءٍ عِلْمًا أَفَلَا
تَتَذَكَّرُونَ ﴿81﴾ وَكَيْفَ أَخَافُ مَا أَشْرَكْتُمْ وَلَا تَخَافُونَ
أَنَّكُمْ أَشْرَكْتُم بِاللَّهِ مَا لَمْ يُنَزِّلْ بِهِ عَلَيْكُمْ سُلْطَٰنًا
فَأَيُّ الْفَرِيقَيْنِ أَحَقُّ بِالْأَمْنِ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿82﴾

75. Ka ambata zamanin da Annabi Ibrahim (Alaihissalamu yake faɗi ga mahaifinsa, wato baffansa (Azaru) "Donme kake riƙon gumaka iyayen giji? Ni ina ganinka da mutanenka a cikin ɓata mabayyani".

76. (Tamfar da muka nuna masa ɓatan baffan nan nasa da mutanensa,) Haka nan muke nuna wa Annabi Ibrahim (Alaihissala-mu,) zuzzurfan mulkin sammai da ƙassai, (donya kafa dalili dashi bisa kaɗaitarmu kuma) donya zama daga cikin masu sakankancewa (da ita).

77. Yayin da dare ya duhunta gareshi sai yaga tauraro, (Ance zara ce,) yace (da mutanensa masa-na taurarin nan) "Wannan shine Ubangijina (a riyawarku?) Yayin da tauraron nan ya faɗi, yace "Ni bana son masu faɗuwa".

78. Yayin dayaga wata ya hudo, sai yace (dasu) 'Yanzu wannan shine Ubangijina? Yayin daya faɗi sai yace "haƙiƙa idan Ubangijina bai shirye ni ba, haƙiƙa zan kasance daga mutaneɓatattu".

79. Yayin daya rana ta hudo, yace "Yanzu wannAnce Ubangijina? Wannan tafi girma (daga tauraro da wata.)" to, yayin data faɗi yace "Yaku mutanena haƙiƙa ni makubuci ne daga abinda kuke shirkanta Allah (dashi, na gumaka da jukkuna fararm, maɓukata izuwa mai faranva (sai sukace dashi to, me kake bautawa,).

80. (Yace) "Haƙiƙa ni na fuskantar da zuciyata ga wanda ya halicci sammai da ƙassai ina mai bi totar! Ni ban kasance daga masu shirkadashi ba",

(JAYAYYAR ANNABI IBRAHIM ALAIHISSALAMU DA MUTANENSA)

81. Mutanensa sun yi jayayya dashi (sun firgita shi da gumaka,) Yacc, "Yanzu kwa dinga jayayya dani a cikin ɗayantakar Allah,alhali Ubangiji ya shirye ni izuwa gare ta, ni bana tsoron abinda kuke shirkanta shi dashi (na gumaka, bazata iyayi mini komai ba saboda batada ikon komai,) sai in Allah yanufi wani abu ne ya same ni, to, wannan kuwa ilimin Ubangijina ya yalwaci komai. Shin kan ba kwa wa'azantu ba.?

82. ƙaƙa zan ji tsoron abinda kuke shirkantawa da Allah (na gumaka, wacce bata cuta bata amfani,) ku ba kwa tsoron Allah cewa ku tara dashi (a cikin bauta) abinda bai saukar da hujja na bautar sa a kanku ba, to, waɗanne jama'a guda biyu ne sukafi cancantada aminci, (mu ko ku,) in kun kasance kun san (wanda yafi cancantar aminci, wanda mune to, kubi shi).

ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَلَمْ يَلْبِسُوٓاْ إِيمَٰنَهُم بِظُلْمٍ اُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلْأَمْنُ
وَهُم مُّهْتَدُونَ ﴿83﴾ وَتِلْكَ حُجَّتُنَآ ءَاتَيْنَٰهَآ إِبْرَٰهِيمَ عَلَىٰ قَوْمِهِۦ
نَرْفَعُ دَرَجَٰتٍ مَّن نَّشَآءُ إِنَّ رَبَّكَ حَكِيمٌ عَلِيمٌ ﴿84﴾
وَوَهَبْنَا لَهُۥٓ إِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ كُلًّا هَدَيْنَا وَنُوحًا هَدَيْنَا
مِن قَبْلُ وَمِن ذُرِّيَّتِهِۦ دَاوُۥدَ وَسُلَيْمَٰنَ وَأَيُّوبَ وَيُوسُفَ
وَمُوسَىٰ وَهَٰرُونَ وَكَذَٰلِكَ نَجْزِي ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿85﴾ وَزَكَرِيَّآءَ
وَيَحْيَىٰ وَعِيسَىٰ وَإِلْيَاسَ كُلٌّ مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿86﴾ وَإِسْمَٰعِيلَ
وَٱلْيَسَعَ وَيُونُسَ وَلُوطًا وَكُلًّا فَضَّلْنَا عَلَى ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿87﴾
وَمِنْ ءَابَآئِهِمْ وَذُرِّيَّٰتِهِمْ وَإِخْوَٰنِهِمْ وَٱجْتَبَيْنَٰهُمْ وَهَدَيْنَٰهُمْ
إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿88﴾ ذَٰلِكَ هُدَى ٱللَّهِ يَهْدِي بِهِۦ مَن يَشَآءُ
مِنْ عِبَادِهِۦ وَلَوْ أَشْرَكُواْ لَحَبِطَ عَنْهُم مَّا كَانُواْ يَعْمَلُونَ ﴿89﴾
اُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ءَاتَيْنَٰهُمُ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحُكْمَ وَٱلنُّبُوٓءَةَ
فَإِن يَكْفُرْ بِهَا هَٰٓؤُلَآءِ فَقَدْ وَكَّلْنَا بِهَا قَوْمًا لَّيْسُواْ بِهَا
بِكَٰفِرِينَ ﴿90﴾ اُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ هَدَى ٱللَّهُ فَبِهُدَىٰهُمُ ٱقْتَدِهْ
قُل لَّآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ أَجْرًا إِنْ هُوَ إِلَّا ذِكْرَىٰ لِلْعَٰلَمِينَ ﴿91﴾

83. (Sai Ubangiji yace,) 'Wađanda suka bada gaskiya basu cuđanya imaninsu dashirka ba, wađancananka sune suke da amincewa daga azaba, sune shiryayyu".

84. Wancananka iTace hujjarmu wadda Annabi Ibrahim (Alaihissalamu) ya kafa hujja da ita (bisa đayantakar Allah, na fađuwar taurari da abinda yake bayansa,) Mun baiwa Annabi Ibrahim (Alaihissalamu) ita a kan mutanensa, muna daukaƙa darjojin wanda mu ka ga dama (a cikin ilmi da hikima). Haƙiƙa Ubangijinka gwanine (cikin aiki) masani (da halitta).

(ANNABI IBRAHIM ALAIHISSLAMU UBAN ANNABAWA DA MARTABARSA)

85. Munbashi Is'haka daya'aƙuba (dansa Alaihimussalam) kowanne daga garesu mun shirye shi. Annabi Nuhu Alaihissalam mun shirye shi tun gaban Annabi Ibrahim (Alaihissalam,) Mun shiryi Annabi Dawuda da Annabi Sulaiman (Alaihimussalam) daga zuriyyar Annabi Nuhu (Alaihissalam,) Mun shiryi Annabi Ayubada Yusufa dan Yaƙuba (Alaihimussalam,) da Annabi Musa da Annabi Haruna (Alaihimussalam,) kamar yadda mukayi musu sakamako muke yi wa wađanda sukayi kyakkyawan aiki.

86. Mun shiryi Annabi Zakariya da Annabi Yahaya dansa (Alaihi-mussalam,) da Annabi Isa Dan Maryama (Alaihimassalam,) da Annabi Iliyasa (Alaihissalam,) (dan Haruna dan uwan Annabi Musa) Kowanne daga cikinsu yana daga cikin salihai.

87. Da Isma'ila dan Ibrahim Alaihis-salam da Alyasa'u da Yunusa dan Mattada LUĐU (dan Harana dan uwa Ibrahima Alaihissalam,) kowanne daga cikinsu munfifita shi a kan mutane da Annabci.

88. Daga iyayensu da zuriyoyinsu da "yan'uwansu, mun zaɓe su mun shiryesu izuwa tafarki madaidaici.

89. Wannan addini da aka shiryesu a kan sa shine addinin Allah, da Allah yake shiriyar wanda yaga dama dashi na daga bayinsa. Dasun yi shirka (takađiri) da aikinsu ya ɓaci ga buransu.

90. Wađancananka sune wađanda muka basu Littattafai da hikima da Annabci. Idan mutanen Makka sun kafirtada ita, wađannan guda uku, to, haƙiƙa mun wakkala mutane da ita, wađanda basu kasance masu kafircewa da ita ba (wato sune Muhajirai da Ansaru).

91. Wađancananka ne wađanda Allah ya shirye su, to, dashiriyarsu na Tauhidi da dauriya, yi koyi dasu, Cene (dasu) "Ni bana tambayar ku Lada bisa ida da aike, (Alƙur'ani). Shi Alƙur'ani bai kasance ba face gargađi ga talikai (aljan da mutane).

ثمن

* وَمَا قَدَرُواْ اُ۬للَّهَ حَقَّ قَدْرِهِۦٓ إِذْ قَالُواْ مَآ أَنزَلَ اَ۬للَّهُ عَلَيٰ
بَشَرٖ مِّن شَےْءٍۖ قُلْ مَنْ أَنزَلَ اَ۬لْكِتَٰبَ اَ۬لذِے جَآءَ بِهِۦ مُوسَيٰ نُوراٗ وَهُديٗ
لِّلنَّاسِۖ تَجْعَلُونَهُۥ قَرَاطِيسَ تُبْدُونَهَا وَتُخْفُونَ كَثِيراٗۖ وَعُلِّمْتُم
مَّا لَمْ تَعْلَمُوٓاْ أَنتُمْ وَلَآ ءَابَآؤُكُمْۖ قُلِ اِ۬للَّهُۖ ثُمَّ ذَرْهُمْ فِے خَوْضِهِمْ
يَلْعَبُونَۖ (92) وَهَٰذَا كِتَٰبٌ أَنزَلْنَٰهُ مُبَٰرَكٞ مُّصَدِّقُ اُ۬لذِے بَيْنَ
يَدَيْهِ وَلِتُنذِرَ أُمَّ اَ۬لْقُرِيٰ وَمَنْ حَوْلَهَاۖ وَالذِينَ يُؤْمِنُونَ بِالَاخِرَةِ
يُؤْمِنُونَ بِهِۦۖ وَهُمْ عَلَيٰ صَلَاتِهِمْ يُحَافِظُونَۖ (93) وَمَنْ أَظْلَمُ
مِمَّنِ اِ۪فْتَرَيٰ عَلَى اَ۬للَّهِ كَذِباً أَوْ قَالَ أُوحِيَ إِلَيَّ وَلَمْ يُوحَ إِلَيْهِ شَےْءٞ
وَمَن قَالَ سَأُنزِلُ مِثْلَ مَآ أَنزَلَ اَ۬للَّهُۖ وَلَوْ تَرَيٰٓ إِذِ اِ۬لظَّٰلِمُونَ
فِے غَمَرَٰتِ اِ۬لْمَوْتِ وَالْمَلَٰٓئِكَةُ بَاسِطُوٓاْ أَيْدِيهِمُۥٓ أَخْرِجُوٓاْ أَنفُسَكُمُۖ
اُ۬لْيَوْمَ تُجْزَوْنَ عَذَابَ اَ۬لْهُونِ بِمَا كُنتُمْ تَقُولُونَ عَلَى اَ۬للَّهِ غَيْرَ اَ۬لْحَقِّ
وَكُنتُمْ عَنَ ـايَٰتِهِۦ تَسْتَكْبِرُونَۖ (94) وَلَقَدْ جِئْتُمُونَا فُرَٰدَيٰ
كَمَا خَلَقْنَٰكُمُۥٓ أَوَّلَ مَرَّةٖ وَتَرَكْتُم مَّا خَوَّلْنَٰكُمْ وَرَآءَ ظُهُورِكُمْۖ
وَمَا نَرَيٰ مَعَكُمْ شُفَعَآءَكُمُ اُ۬لذِينَ زَعَمْتُمُۥٓ أَنَّهُمْ فِيكُمْ شُرَكَٰٓؤُاْۖ
لَقَد تَّقَطَّعَ بَيْنَكُمْ وَضَلَّ عَنكُم مَّا كُنتُمْ تَزْعُمُونَۖ (95)

(TABBATAR DA MANZANTAKAR MA'AIKI DA TASIRINTA)

92. Yahudu basu ba Allah girma gwargwadon gimiansa ba, zam-anin da suka faɗa (ga Manzon Aliah Sallallahu alaihi wasallama, alhali sun yi jayayya dashi a cikin Alƙur'am). "Allah bai saukar da komai bisa ɗan taliki ba".Cene (dasu) "Wa ya saukar da Littafin da Annabi Musa yazo dashi? Haske dashiriyaga mutane, kuma Ya sanyashi takardu (ku na rubuta shi cikin dabtarori ababan daddatsawa). Kuna bayyana abinda kuka ga damar bayyana shi, kuna ɓoye mai yawa daga abinda yake cikinta, kamar kamannin Annabi Sallallahu alaihi wasallama. An sanar da ku, ku Yahudu a cikin Alƙur'ani abinda baku sani ba, ku wala iyayenku,, na Labarin Attaura da bayanin abinda ya rikita agarekuda abinda akayi sabani a kai). To, cene Allah ne ya saukar dashi, sannan ka rabu dasu suyi wasa a cikin kutsaw-arsu a cikin aikin banza.
93. Wannan alƙur'ani Littafi ne Allah ya saukar dashi mai albarka, mai gasgata abinda yake gabansa na Littattafai, donka tsoratar da uwar alƙaryu (iTace Makka da abinda yake daura da ita na daga sauran mutane, har izuwa ƙarshen bangon duniya). Waɗanda suka bada gaskiya da ranar Lahira suna bada gaskiya dashi, su masu kaffa- kaffa ne a kan sallarsu (don tsoron azabar Allah)

(ƘARYAGA ALLAH DA SAKAMAKONTA)

94. Ba mafi zalunci ga wanda ya ƙirƙiri ƙarya bisa Ubangiji, (da da'awar Annabci,) alhali ba annabi ne bako yace "An aiko izuwa gareshi alhali ba a aiko komai ba izuwa gareshi. (Ta sauka cikin Musailama) da Wanda yace "Da sannu zan saukar da misalin abinda Allah ya saukar, masu izgili ke nan. Da kana gani (Ya Muhammadu Sallallahu alaika wasallama zamanin da azzalumai suke cikin magagin mutuwa, ga Mala'iku suna shinfiɗe hannunsu izuwa garesu (da ɗuka da azaba, suna faɗa musu don muzantawa a garesu,) Ku fito da kawukanku)izuwa garemu don mu karɓa,) a yau ne za a saka muku azabar wulaƙanci, saboda kuna faɗar ƙaryaga Allah, kuma kun kasance masu girman kai (ga buran ayoyinmu, daka ga al'amari maigirma).
95. Haƙiƙa kun zo mana ɗai - ɗai kamar yadda muka halicce ku marrar farko, marasa takalma matsiraita marasa sha. masu loɓa, kun bar abinda muka baku (na daga dukiya) bayan bayanku, (ana cewa dasu don woho a garesu,) Barna ganin su masu ceton nan naku taredaku ,(sune gumaka,) kuka riga cewa su masu tarayya ne (da Allah a cikin cancantar bauta tsakaninku, haƙiƙa tsakaninku ya yan-yanke, abinda kuke riyawa a duniya na ceton ta ya guje muku.

رُبع
۞ إِنَّ ٱللَّهَ فَٰلِقُ ٱلْحَبِّ وَٱلنَّوَىٰ ۖ يُخْرِجُ ٱلْحَىَّ مِنَ ٱلْمَيِّتِ وَمُخْرِجُ
ٱلْمَيِّتِ مِنَ ٱلْحَىِّ ۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ ۖ فَأَنَّىٰ تُؤْفَكُونَ ﴿96﴾ فَالِقُ ٱلْإِصْبَاحِ
وَجَعَلَ ٱلَّيْلَ سَكَنًا وَٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ حُسْبَانًا ۚ ذَٰلِكَ تَقْدِيرُ
ٱلْعَزِيزِ ٱلْعَلِيمِ ﴿97﴾ وَهُوَ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ ٱلنُّجُومَ لِتَهْتَدُوا۟ بِهَا
فِى ظُلُمَٰتِ ٱلْبَرِّ وَٱلْبَحْرِ ۗ قَدْ فَصَّلْنَا ٱلْءَايَٰتِ لِقَوْمٍ يَعْلَمُونَ ﴿98﴾
وَهُوَ ٱلَّذِىٓ أَنشَأَكُم مِّن نَّفْسٍ وَٰحِدَةٍ فَمُسْتَقَرٌّ وَمُسْتَوْدَعٌ ۗ
قَدْ فَصَّلْنَا ٱلْءَايَٰتِ لِقَوْمٍ يَفْقَهُونَ ﴿99﴾ وَهُوَ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ مِنَ
ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَخْرَجْنَا بِهِۦ نَبَاتَ كُلِّ شَىْءٍ فَأَخْرَجْنَا مِنْهُ خَضِرًا
نُّخْرِجُ مِنْهُ حَبًّا مُّتَرَاكِبًا وَمِنَ ٱلنَّخْلِ مِن طَلْعِهَا قِنْوَانٌ دَانِيَةٌ
وَجَنَّٰتٍ مِّنْ أَعْنَابٍ وَٱلزَّيْتُونَ وَٱلرُّمَّانَ مُشْتَبِهًا وَغَيْرَ مُتَشَٰبِهٍ ۗ
ٱنظُرُوٓا۟ إِلَىٰ ثُمُرِهِۦٓ إِذَآ أَثْمَرَ وَيَنْعِهِۦٓ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكُمُۥ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ
ثُمن
يُؤْمِنُونَ ﴿100﴾ ۞ وَجَعَلُوا۟ لِلَّهِ شُرَكَآءَ ٱلْجِنَّ وَخَلَقَهُمْ ۖ وَخَرَّقُوا۟ لَهُۥ
بَنِينَ وَبَنَٰتٍۭ بِغَيْرِ عِلْمٍ ۚ سُبْحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يَصِفُونَ ﴿101﴾
بَدِيعُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ أَنَّىٰ يَكُونُ لَهُۥ وَلَدٌ وَلَمْ تَكُن لَّهُۥ
صَٰحِبَةٌ ۖ وَخَلَقَ كُلَّ شَىْءٍ ۖ وَهُوَ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿102﴾

(WANI ABU DAGA AL' AMARIN IKON ALLAH DA ILIMINSA DA HIKIMARSA DA RAHAMARSA)

96. Haƙiƙa Ubangiji mai tsaga kwaya ne ga tsiri da ɗan ɓalle ga dabino, yana fitar da rayayye daga matacce (kamar mutum da tsuntsu daga maniyyi da kwai,) yana fitar da matacce daga mai rai, wancananku mai tsagawar nan da fitarwa Allah ke nan, to, yaya ake juyar daku ,(ga buran imani tareda bayyanar burhani).

97. Mai keto al'amudin asubahi, (shine farkon abinda yake bayyana na hasken rana ga duhun dare) (shine alfijir maƙaryaci wanda magasgacin yake bin sa) mai sanya dare mahutar bawa (daga wahala,) mai sanya rana da wata kidaya (ga Lokatai,) Wancananka abin ambato, kaddarawar mabuwayi ne masani (da halitta).

98. Shine wanda yasanya muku taurari domin ku shiryu da ita a cikin duffan sarari dana kogi, (a cikin tafiyetafiye,) haƙiƙa munyi bayanin ayoyi (masu nuna ikonmu) ga mutane ma'abuta Lura.

99. Shine wanda ya fare ku daga rai guda ɗaya (wato Annabi Adamu Alaihissalam,) to, matabbaci daga gareku a cikin mahaifa da gurin ajiya daga gareku a wurin tsatso. Haƙiƙa mun rarrabe ayoyi ga mutane masu fahinta.

100. Shine wanda ya saukar da ruwa daga sama, muka fitar da tsirin kowane abu da ruwan nan muka fitar da kore daga tsirin nan, muna fitarwa da ƙwaya daga koren nan mai hauhawar juna ba'alinsa yana hawa ba'ali kamar zangarniyar alkama, daga dabino akwai dunsai daga hu-darta makusantada juna, muka fitar da gonakai na inabai da zaitun da rumman marikicin ganye da wanin marikicin itaciya. (Yaku waɗanda muke zance da ku) kuyi duba izuwa "ya" yan itaciyarsa idan ya fara nuna yaya yake kuma ku duba izuwa nunar sa yaya yake, haƙiƙa a cikin wancananka akwai ayoyi (masu nuna ikon Allah a bisa tashin alƙiyama da waninsa) a kan mutane masu tsoron Allah.

(ƘARYAR MUSHIRIKAI GA ALLAH DA RADDI A KANSU)

101. Sun sanyawa Ubangiji sharikai, aljannu, (yayin da sukabi su a cikin bautar gumaka) alhali kuma Ubangiji ne ya halicce su, ƙaƙa zasu zama sharikansa, sun ƙago masa "ya" yaye maza da mata bada ilimi ba, (sukace Uzairu ɗan Allah ne kuma Mala'iku "ya" yan Allah ne, wato Yahudu sunce Uzairu ɗan Allah, Nasara sunce Almasihu ɗan Allah ne, mushirikai sunce Mala'iku "ya" yan Allah ne). Tsarki ya tabbata gareshiya girma ga buran abinda suke sufanta shi (dashi na daga ɗa).

102. Shine mai ƙagar sammai da ƙassai bada misali daya rigaya ba, yaya ɗa zai kasance gareshi, alhali ba mace a gareshi, Ya halicci kowane abu (wanda sha'aninsa a halicce shi). Shi masanine da komai.

ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمْ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ خَٰلِقُ كُلِّ شَيْءٖ فَٱعْبُدُوهُ
وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٖ وَكِيلٞ ﴿103﴾ لَّا تُدْرِكُهُ ٱلْأَبْصَٰرُ
وَهُوَ يُدْرِكُ ٱلْأَبْصَٰرَ وَهُوَ ٱللَّطِيفُ ٱلْخَبِيرُ ﴿104﴾ قَدْ جَآءَكُم
بَصَآئِرُ مِن رَّبِّكُمْ فَمَنْ أَبْصَرَ فَلِنَفْسِهِۦ وَمَنْ عَمِيَ فَعَلَيْهَا
وَمَآ أَنَا۠ عَلَيْكُم بِحَفِيظٖ ﴿105﴾ وَكَذَٰلِكَ نُصَرِّفُ ٱلْآيَٰتِ
وَلِيَقُولُواْ دَرَسْتَ وَلِنُبَيِّنَهُۥ لِقَوْمٖ يَعْلَمُونَ ﴿106﴾ ٱتَّبِعْ مَآ أُوحِيَ
إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَأَعْرِضْ عَنِ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿107﴾
وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَآ أَشْرَكُواْ وَمَا جَعَلْنَٰكَ عَلَيْهِمْ حَفِيظٗا وَمَآ أَنتَ
عَلَيْهِم بِوَكِيلٖ ﴿108﴾ وَلَا تَسُبُّواْ ٱلَّذِينَ يَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ
فَيَسُبُّواْ ٱللَّهَ عَدْوَۢا بِغَيْرِ عِلْمٖ كَذَٰلِكَ زَيَّنَّا لِكُلِّ أُمَّةٍ
عَمَلَهُمْ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّهِم مَّرْجِعُهُمْ فَيُنَبِّئُهُم بِمَا كَانُواْ يَعْمَلُونَ ﴿109﴾
وَأَقْسَمُواْ بِٱللَّهِ جَهْدَ أَيْمَٰنِهِمْ لَئِن جَآءَتْهُمْ ءَايَةٞ لَّيُؤْمِنُنَّ بِهَا
قُلْ إِنَّمَا ٱلْآيَٰتُ عِندَ ٱللَّهِ وَمَا يُشْعِرُكُمْ أَنَّهَآ إِذَا جَآءَتْ
لَا يُؤْمِنُونَ ﴿110﴾ وَنُقَلِّبُ أَفْـِٔدَتَهُمْ وَأَبْصَٰرَهُمْ كَمَا لَمْ يُؤْمِنُواْ
بِهِۦٓ أَوَّلَ مَرَّةٖ وَنَذَرُهُمْ فِي طُغْيَٰنِهِمْ يَعْمَهُونَ ﴿111﴾

103. Wancananku Allah ke nan Ubangijinku, babu abin bautawa da gaskiya sai shi, mahalaccin kowanne abu ku bauta masa ku kađaita shi, shi wakiline shi bisa komai.

104. Idanuwa basa kewayewa dashi, shine yake riskar idanuwa, shine mai taushi mai cikakken sani.

(HAƘƘOƘI DA SUKA RATAYA DA AIKE)

105. Haƙiƙa hujjoji sun zo muku daga Ubangijinku, to, wanda yaganta (ya bada gaskiya,) to, yayi ga kansa, wanda kuma ya makance ga buranta (ya ɓata,) to, ya cuci kansa, ni ban kasance mai tsaro a kan ku ba.

106. Kamar yadda mukayi bayanin abinda muka bayyana maka haka muke bayyana ayoyi don ayi izna kuma don kafirai su fađa su ce, wato ka dosani sani daga mazowa Littafi, kuma don mu bayyana shi ga mutane ma'abuta sani.

107. Bi abinda aka aiko zuwa gareka daga Ubangijinka, (shine Alƙur'ani) babu abin bautawa da gaskiya sai shi, rabu da mushirikai.

108. Da Allah ya nufa da baza suyi shirka ba, Bamu sanya ka mai tsaro a kansu ba, kai ba wakili ne a kan su ba (balle ka tilashe su a kan imani).

(HANI GA ZAGIN Wađanda suke BAUTAWA WANIN ALLAH)

109. Kadaku ,zagi wađanda suke bautawa ba Allah ba, (sune gumaka,) saisu zagi Ubangiji don shisshigi, bada ilimi ba (saboda jahilcinsu da Allah,) tamfar da muka zayyana wa wađannan abindasu suke kansa, haka nan muka kewatawa kowacce al'umma ayyukanta (na hairi ko sharri,) sannan izuwa Ubangijinsu zasu koma ranar alƙiyama ya basu Labarin abinda suke aikatawa.

110. Sun rantse da Allah iyakacin rantsu warsu kafiran Makka, Wallahi idan aya tazo musu (daga abinda suka ƙaga,) Lallai zasu bada gaskiya da ita. Cene (dasu) ai ayoyi dai suna gun Allah, bai sanar daku ,ba cewa haƙiƙa ita idan tazo bazasu bada gaskiya ba.

111. Muna juya zukatansu da idanuwansu (ga buran gaskiya, bazasu ga gaskiyaba bazasu bada gaskiya bakamar yadda basu bada gaskiya dashi ba a marrar farko ba tambar da basu bada gaskiye da abinda aka sau kar musu marrar farko ba., zamu barsu a cikin shisshiginsu suna yin kai - kawo.

حزب

۞ وَلَوْ أَنَّنَا نَزَّلْنَا إِلَيْهِمُ الْمَلَـٰٓئِكَةَ وَكَلَّمَهُمُ الْمَوْتَىٰ وَحَشَرْنَا
عَلَيْهِمْ كُلَّ شَيْءٍ قِبَلًا مَّا كَانُوا لِيُؤْمِنُوا إِلَّا أَن يَشَاءَ اللَّهُ
وَلَـٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ يَجْهَلُونَ ﴿١١١﴾ وَكَذَٰلِكَ جَعَلْنَا لِكُلِّ نَبِيٍّ عَدُوًّا
شَيَـٰطِينَ الْإِنسِ وَالْجِنِّ يُوحِي بَعْضُهُمْ إِلَىٰ بَعْضٍ زُخْرُفَ الْقَوْلِ
غُرُورًا وَلَوْ شَاءَ رَبُّكَ مَا فَعَلُوهُ فَذَرْهُمْ وَمَا يَفْتَرُونَ ﴿١١٢﴾
وَلِتَصْغَىٰ إِلَيْهِ أَفْـِٔدَةُ الَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِالْآخِرَةِ
وَلِيَرْضَوْهُ وَلِيَقْتَرِفُوا مَا هُم مُّقْتَرِفُونَ ﴿١١٣﴾ أَفَغَيْرَ اللَّهِ
أَبْتَغِي حَكَمًا وَهُوَ الَّذِي أَنزَلَ إِلَيْكُمُ الْكِتَـٰبَ مُفَصَّلًا
وَالَّذِينَ ءَاتَيْنَـٰهُمُ الْكِتَـٰبَ يَعْلَمُونَ أَنَّهُ مُنَزَّلٌ مِّن رَّبِّكَ
بِالْحَقِّ فَلَا تَكُونَنَّ مِنَ الْمُمْتَرِينَ ﴿١١٤﴾ وَتَمَّتْ كَلِمَتُ رَبِّكَ
صِدْقًا وَعَدْلًا لَّا مُبَدِّلَ لِكَلِمَـٰتِهِ وَهُوَ السَّمِيعُ الْعَلِيمُ ﴿١١٥﴾
وَإِن تُطِعْ أَكْثَرَ مَن فِي الْأَرْضِ يُضِلُّوكَ عَن سَبِيلِ اللَّهِ
إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا الظَّنَّ وَإِنْ هُمْ إِلَّا يَخْرُصُونَ ﴿١١٦﴾ إِنَّ رَبَّكَ
هُوَ أَعْلَمُ مَن يَضِلُّ عَن سَبِيلِهِ وَهُوَ أَعْلَمُ بِالْمُهْتَدِينَ ﴿١١٧﴾ فَكُلُوا
مِمَّا ذُكِرَ اسْمُ اللَّهِ عَلَيْهِ إِن كُنتُم بِـَٔايَـٰتِهِ مُؤْمِنِينَ ﴿١١٨﴾

112. Da haƙiƙa cewa mu mun saukar da Mala'iku izuwa garesu, ko matattu sukayi zance dasu (tamfar du suka shifto,) muka tara musu kowane abu karara, (suka shaida da gaskiyar ka,) bazasu kasance masu gasgatawa ba (saboda abinda ya rigaya a cikin sanin Allah,) sai ko in Allah ya nufa, amma yawaicinsu sunjahilci (haka).

113. (Tamfar da muka sanya waɗannan magautanka,) hakana muka sanya magauci ga kowane Annabi, shaiɗanun mutane dana aljanu, ba'alinsu yana kim-sawar .maganar banza izuwa ba'ali don ruɗi, (ai donsu ruɗe su.) Da Ubangijinka yaga dama da basu aikata cusawar nan ba, to barsu da abinda suke ƙirƙira na kafirci da waninsa daga abinda aka ƙawata musu, (wannan gaban umarni dayaƙi ne).

114. Kuma don zukatan waɗanda basu bada gaskiya da ranar Lahira bata karkata izuwa cusawar banzan nan, kuma donsu yarda dashi su tsuwurwuci abinda suke tsuwurwurta na daga zunubai don ayi musu azabadashi.

KO TUN.MAN ZON ALLAH (S.A.W) SHINE KADAI BABBAN KOTU NA DAUKAKA KARA SHINE KUMA MAJA LISAR, DIN KIN DUNIYA.)

Yayin da suka nemi Annabi yasan-ya musu alƙalin daukaka ƙara sai Allah yace':

115. A'a Wanin Allah zan sanya alkati tsakanina da ku, alhali shine wanda ya saukar da Littafi a gareku (shine alƙur'ani) abin rarrabewa, mai bayyanawar ƙarya da gaskiya. Waɗanda muka basu Littafi (Attaura kamar Abdullahi Bini Salami da abokansa) sunsan cewa shi haƙiƙa abin saukarwa ne daga Ubangijinka da gaskiya, to, kadaka kasance daga masuyin kokwanto a kansa (ana tabbatar wa da kafirai) gaskiyar alƙur'ani ne, wato zance dashi yake amma kafirai yake nufi.

116. Kalmomin Ubangijinka (na hu-kunce - hukunce da gargaɗe -gargaɗe) sune cikar gaskiya da adalci, ba mai misanyawa ga kalmomin Ubangiji, shine mai ji mai sani.

(ƘUDIRE - ƘUDIREN MUSHIRIKAI DAYANKE - YANKENSU)

117. Idan ka biye wa yawaicin waɗanda suke bayan ƙasa na kafirai sa ɓatar dakai ga buran addinin Allah, basa bin komai (cikin jayayyarsu dakai a cikin sha'anin mushe) sai zato, (dasuke cewa wai abinda Allah ya kashe yafi kyau a ci daga abinda mutum ya kashe,) su basu kasance a cikin wannan face maƙaryata.

118. Haƙiƙa Ubangijinka shine masani da wanda yake ɓacewa ga buran addininsa, shine kuma masani da masu shiriya.

119. Kuci daga abinda aka ambaci sunan Allah a kansa (yayin yankansa) in kun kasance masu bada gaskiya da ayoyinsa.

وَمَا لَكُمُۥٓ أَلَّا تَأْكُلُواْ مِمَّا ذُكِرَ اسْمُ اللَّهِ عَلَيْهِ وَقَدْ فَصَّلَ
لَكُم مَّا حَرَّمَ عَلَيْكُمُۥٓ إِلَّا مَا اضْطُرِرْتُمُۥٓ إِلَيْهِ وَإِنَّ كَثِيرًا
لَّيُضِلُّونَ بِأَهْوَآئِهِم بِغَيْرِ عِلْمٍ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعْلَمُ بِالْمُعْتَدِينَ ﴿120﴾
* وَذَرُواْ ظَاهِرَ الْإِثْمِ وَبَاطِنَهُۥٓ إِنَّ الَّذِينَ يَكْسِبُونَ الْإِثْمَ ثمن
سَيُجْزَوْنَ بِمَا كَانُواْ يَقْتَرِفُونَ ﴿121﴾ وَلَا تَأْكُلُواْ مِمَّا لَمْ يُذْكَرِ اسْمُ
اللَّهِ عَلَيْهِ وَإِنَّهُۥ لَفِسْقٌ وَإِنَّ الشَّيَٰطِينَ لَيُوحُونَ إِلَىٰٓ
أَوْلِيَآئِهِمْ لِيُجَٰدِلُوكُمْ وَإِنْ أَطَعْتُمُوهُمُۥٓ إِنَّكُمْ لَمُشْرِكُونَ ﴿122﴾
أَوَمَن كَانَ مَيْتًا فَأَحْيَيْنَٰهُ وَجَعَلْنَا لَهُۥ نُورًا يَمْشِي بِهِۦ
فِي النَّاسِ كَمَن مَّثَلُهُۥ فِي الظُّلُمَٰتِ لَيْسَ بِخَارِجٍ مِّنْهَا
كَذَٰلِكَ زُيِّنَ لِلْكَٰفِرِينَ مَا كَانُواْ يَعْمَلُونَ ﴿123﴾ وَكَذَٰلِكَ
جَعَلْنَا فِي كُلِّ قَرْيَةٍ أَكَٰبِرَ مُجْرِمِيهَا لِيَمْكُرُواْ فِيهَا
وَمَا يَمْكُرُونَ إِلَّا بِأَنفُسِهِمْ وَمَا يَشْعُرُونَ ﴿124﴾ وَإِذَا
جَآءَتْهُمُۥٓ ءَايَةٌ قَالُواْ لَن نُّؤْمِنَ حَتَّىٰ نُؤْتَىٰ مِثْلَ مَآ أُوتِيَ رُسُلُ
اللَّهِ اللَّهُ أَعْلَمُ حَيْثُ يَجْعَلُ رِسَٰلَتَهُۥ سَيُصِيبُ الَّذِينَ أَجْرَمُواْ
صَغَارٌ عِندَ اللَّهِ وَعَذَابٌ شَدِيدٌ بِمَا كَانُواْ يَمْكُرُونَ ﴿125﴾

120. Meye garekuda bazaKuci daga abinda aka ambaci sunan Allah a kansa ba, (na daga yanke - yanke,) alhali ya rabe muku abinda ya haramta gareku (a cikin ayar HURRIMAT ALAIKUMUL MAITATA sai abinda kuka tilasu izuwa gareshi, (to, wannan halal ne gareku,) haƙiƙa yawaici suna ɓata saboda soye soyen zukatansu (saboda halatta mushe da waninsa) ba tareda ilimi (da suka dogara kansa ba). To, haƙiƙa Ubangijinka shine masani da masu shisshigi (ƙetare halal izuwa haram).

(MAFI MAHIMMANCIN SHARAɗIN SUFAYE)

121. Ku bar zahirin zunubi da baɗininsa, (wato ku bar dukkan sabo na sarari dana ɓoye,) Waɗanda suke tsuwurwurtar zunubi da sannu Za a saka musu a Lahira da abinda suka kasance suna aikatawa (a duniya).

(WAJABCIN AMBATON SUNAN ALLAH YAYIN YANKA)

122. Kadaku ,ci daga abinda ba a ambaci sunan Allah a kansa ba, haƙiƙa wannan ci daga mushe fasiƙanci ne, haƙiƙa shaiɗanu suna kimsa wa waliyyansu (kafirai, suna kimsa musu wuswasi,) donsuyi jayayya daku, (cikin halatta mushe,) idan kun biye musu, haƙiƙa ku Lallai mushirikai ne.

(MISALIN MUMINI DA KAFIRI)

Wannan ta sauka a cikin Abi jahal da waninsa'.

123. Yanzu wanda ya kasance matacce da kafirci muka raya shi dashiriya muka sanya masa haske da yake tafiya dashi (cikin mutane,) zai zamo kamar wanda misalinsa a cikin duffai bazai fita daga gareta ba, (shine kafiri, a'a',) to, tamfar da muka kawatawa muminai imani muke kawatawa kafirai abinda suka kasance suna aikatawa (na kafirci da sabo).

124. (Kuma kamar yadda muka sanya fasiƙan Makka manyan ta,) hakana muka sanya a cikin kowace alƙarya manya manyan masu Laifinta, ƙarshen al'amarinsu suyi makirci a cikinta, basuna makirtar kowa bane sai kansu, amma basu san haka ba.

(RUƊIN MUSHIRIKAI DA AƘIBARSU)

125. Idan Aya ta zowa mutanen Makka (bisa gaskiyar ma'aiki alaihissalam) sukAnce "Bazamu gaskata dashi ba, sai an bamu misalin abinda ake baiwa manzannin Allah" (na daga aike da wahayi izuwa garemu saboda a faɗarsu sun fi shi yawan dukiya, sun fi shi yawan shekaru gamɓashai)[1] Allah ne yasan indazai ajiye jakadancinsa, da sannu wulakanci zai sami waɗanda sukayi katoɓarar nan da azaba mai tsanani (saboda makircinsu).

1) Wato wawaye.

فَمَنْ يُّرِدِ اللَّهُ أَنْ يَّهْدِيَهُۥ يَشْرَحْ صَدْرَهُۥ لِلْإِسْلَامِ وَمَنْ
يُّرِدْ أَنْ يُّضِلَّهُۥ يَجْعَلْ صَدْرَهُۥ ضَيِّقاً حَرِجاً كَأَنَّمَا يَصَّعَّدُ فِي السَّمَآءِ
كَذَٰلِكَ يَجْعَلُ اللَّهُ الرِّجْسَ عَلَى الَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿126﴾ وَهَٰذَا صِرَاطُ
رَبِّكَ مُسْتَقِيماً قَدْ فَصَّلْنَا الْآيَاتِ لِقَوْمٍ يَذَّكَّرُونَ ﴿127﴾
ربع
* لَهُمْ دَارُ السَّلَامِ عِنْدَ رَبِّهِمْ وَهُوَ وَلِيُّهُم بِمَا كَانُوا يَعْمَلُونَ ﴿128﴾
وَيَوْمَ نَحْشُرُهُمْ جَمِيعاً يَٰمَعْشَرَ الْجِنِّ قَدِ اسْتَكْثَرْتُم مِّنَ الْإِنسِ
وَقَالَ أَوْلِيَآؤُهُم مِّنَ الْإِنسِ رَبَّنَا اسْتَمْتَعَ بَعْضُنَا بِبَعْضٍ وَبَلَغْنَا
أَجَلَنَا الَّذِي أَجَّلْتَ لَنَا قَالَ النَّارُ مَثْوَاكُمْ خَٰلِدِينَ فِيهَا
إِلَّا مَا شَآءَ اللَّهُ إِنَّ رَبَّكَ حَكِيمٌ عَلِيمٌ ﴿129﴾ وَكَذَٰلِكَ نُوَلِّي
بَعْضَ الظَّٰلِمِينَ بَعْضاً بِمَا كَانُوا يَكْسِبُونَ ﴿130﴾ يَٰمَعْشَرَ
الْجِنِّ وَالْإِنسِ أَلَمْ يَأْتِكُمْ رُسُلٌ مِّنكُمْ يَقُصُّونَ عَلَيْكُمْ
ءَايَٰتِي وَيُنذِرُونَكُمْ لِقَآءَ يَوْمِكُمْ هَٰذَا قَالُوا شَهِدْنَا
عَلَىٰ أَنفُسِنَا وَغَرَّتْهُمُ الْحَيَوٰةُ الدُّنْيَا وَشَهِدُوا عَلَىٰ
أَنفُسِهِمْ أَنَّهُمْ كَانُوا كَٰفِرِينَ ﴿131﴾ ذَٰلِكَ أَن لَّمْ يَكُن
رَّبُّكَ مُهْلِكَ الْقُرَىٰ بِظُلْمٍ وَأَهْلُهَا غَٰفِلُونَ ﴿132﴾

(AL'ADAR ALLAH CIKIN HALITTADA ADDININSA NA GASKIYA)

126. Wanda Allah yayi nufin ya shirye shi saiya buđ e kirjinsa da Musulunci, (shine ya jefa haske a cikin zuciyarsa, saiya buđu gareshiya karɓe shi tamfar dayazo a cikin Hadisi) Wanda Allah yanufi ɓasshe shi sai yasanya ƙirjinsa ƙunƙunta gam, (Yakulle shi) kai kace yana hawa a cikin sama in an kallafa masa imani. Tamfar irin wannan sanyawa Allah yake sanya azaba a kan wadanda basu bada gaskiya ba.

127. Wannan abinda kake kansa (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama,) hanyar Ubangijinka ne totar. Haƙiƙa munyi bayanin ayoyi ga mutane masu wa'azantuwa (saboda sun e masu amfani dashi).

128. Gidan aminci na garesu a aljanna nan ga Ubangijinsa shine majiɓincinsu saboda abinda suka kasance suna aikatawa.

129. Ambaci ranar da muke tara su baki đaya (a ce dasu) "Yaku taron aljannu, haƙiƙa kun yawaita daga halakar da "yan Adam. Manya - manyansu na daga '"yan Adam Sukace, Ya Ubangijinmu ba'alinmu yaji dađi da ba'ali, (wato mutane sun amfana da kawata sha'awace -sha'awace da shaiđanu sukayi musu, shaiđanu sun amfana da biyayyar da mutane sukayi musu) mun isa ajalinmu wandaka iyakance mana shine ranar Alƙiyama, (sun fađi wannan ne don nadama)". Ubangiji yace (dasu a bisa harshen Mala'iku); "WuTace makomarku baki-đaya, madauwama a cikinta sai abinda Allah yaga dama (na daga Lokatai da zasu fita daga ciki don shan tafashsshen ruwa a wajen jahannama)". Haƙiƙa Ubangijinka gwanine cikin aiki, masani da halitta.

(WANI ABU DAGA AL'ADAR ALLAH A CIKIN HALITTA TAREDA SASHEN MATSAYAN LAHIRA)

130. Tamfar da muka jiyar da masu saɓo na mutane da aljannu dađi muka sallađa ba'alin azzalumai a kan ba'ali. (maganin biri karen maguzawa) saboda abinda suka kasance suna aikatawa na sabo.

131. Yaku jama'ar aljannu da mutane, shin manzanni daga gareku basu zo muku bane suna Labarta muku ayoyina? (Wato jakadun aljannu su ne muƙaddasai dasuke jiyo maganar manzannisu na mutane sannan su isar izuwa "yan uwansu don Ubangiji bai yiwo rasuli a cikinsu ba) suna tsoratar daku ,saduwa da ranarku wannan, suka ce; "Mun shaida a bisa kawunanmu (cewa sun iyar mana". Ubangiji yace; rayuwar duniya ta ruđe su (saboda haka basu bada gaskiya ba). Suka shaida a kan kansu cewa haƙiƙa su sun tabbata kafirai.

132. Aiko manzannin nan saboda cewa Ubangijinka ba mai halakar da alƙaryabane saboda zalunci daga gareta alhali Allah bai aiko da jakada ga mutanenta ba.

وَلِكُلٍّ دَرَجَٰتٌ مِّمَّا عَمِلُواْ وَمَا رَبُّكَ بِغَٰفِلٍ عَمَّا
يَعْمَلُونَ ﴿133﴾ وَرَبُّكَ ٱلْغَنِيُّ ذُو ٱلرَّحْمَةِ إِن يَشَأْ
يُذْهِبْكُمْ وَيَسْتَخْلِفْ مِنۢ بَعْدِكُم مَّا يَشَآءُ
كَمَآ أَنشَأَكُم مِّن ذُرِّيَّةِ قَوْمٍ ءَاخَرِينَ ﴿134﴾ إِنَّ مَا
تُوعَدُونَ لَءَاتٍ وَمَآ أَنتُم بِمُعْجِزِينَ ﴿135﴾ قُلْ يَٰقَوْمِ
ٱعْمَلُواْ عَلَىٰ مَكَانَتِكُمْ إِنِّي عَٰمِلٌ فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ
مَن تَكُونُ لَهُۥ عَٰقِبَةُ ٱلدَّارِ إِنَّهُۥ لَا يُفْلِحُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿136﴾
۞ وَجَعَلُواْ لِلَّهِ مِمَّا ذَرَأَ مِنَ ٱلْحَرْثِ وَٱلْأَنْعَٰمِ نَصِيبًا ثُمُن
فَقَالُواْ هَٰذَا لِلَّهِ بِزَعْمِهِمْ وَهَٰذَا لِشُرَكَآئِنَا
فَمَا كَانَ لِشُرَكَآئِهِمْ فَلَا يَصِلُ إِلَى ٱللَّهِ
وَمَا كَانَ لِلَّهِ فَهُوَ يَصِلُ إِلَىٰ شُرَكَآئِهِمْ
سَآءَ مَا يَحْكُمُونَ ﴿137﴾ وَكَذَٰلِكَ زَيَّنَ لِكَثِيرٍ مِّنَ
ٱلْمُشْرِكِينَ قَتْلَ أَوْلَٰدِهِمْ شُرَكَآؤُهُمْ
لِيُرْدُوهُمْ وَلِيَلْبِسُواْ عَلَيْهِمْ دِينَهُمْ وَلَوْ شَآءَ
ٱللَّهُ مَا فَعَلُوهُ فَذَرْهُمْ وَمَا يَفْتَرُونَ ﴿138﴾

133. Kowa ne daga ma'aikata suna da sakamako daga abinda suka aikata (na sharri ko hairi). Ubangijinka ba marabkanine ga buran aikin bayi ba.

(BAN TSORO DA GARGADI)

134. Ubangijinka shine mawadaci (ga buran halittada bautarsu) mai rahama. In yaga dama saiya halakar daku ,Yaku mutanen makka ya mayar da abinda yaga dama na halitta bayanku, tamfar daya fare ku daga zuriyar waɗansu mutane dabam, sai dai ya wanzar daku ,ne don rahama gareku.
135. Haƙiƙa abinda ake yi muku alwashi (na alƙiyama mai zuwa ne. Ku ba masu tsere wa Allah ne ba.
136. Cene (dasu) "Yaku mutanena kuyi aiki a kan halinku, haƙiƙa ni mai aiki ne a kan halina. Da sannu zaku ga wanda kyakkyawar makoma zata kasance gareshi (mu ko ku). Haƙiƙa azzalumai bazasu azurta ba".

(WANI ABU DAGA HALIN JAHILIYYA NA FARKO DA TSARIN IYAYI)

137. Kafiran Makka sunsanya rabo (dasuke gabatar dashi izuwa baƙi da musakai, kuma sun sanya rabo dasuke gabatar dashi izuwa masuyi musu hidima, sun sanya wa Allah shi daga abinda ya halitta na hatsi da dabbobi,) suka ce; "Wannan na Allah ne don riyawarsu, wannan na gumakanmu ne" (sun kasance idan wani abu na nasibin Allah ya faɗa cikinta saisu tsince, idan wani abu ya faɗa na nasibinsa cikin na gumaka, saisu bar shi su ce Allah mawadaci ne ga buran wannan, sai Ubangiji yace,) "Abinda ya kasance izuwa gumakansu bazai sadu izuwa Allah ba, abinda ya zama na Allah to, shiya kasance yana saduwa izuwa gumakansu, tir, da wannan hukunci nasu".
138. Tamfar da aka ƙawata musu abinda aka ambata shumagabanninsu na aljannu suka ƙawata wa yawaicin mushirikai binne "ya" yayansu da ransu, (wato abinda mutane suke a yanzu na shan magani) donsu rage "ya" ya (yana daga cikin wannan kisa da Allah yake faɗa. Bai halatta Musulmi ya sha magani donya rage haihuwa ba donsu halakar dasu) su rikita musu addininsu. Da Allah yaga dama bazasu aikata haka ba. To, barsu da abinda suke ƙirƙira.

وَقَالُواْ هَٰذِهِۦٓ أَنْعَٰمٌ وَحَرْثٌ حِجْرٌ لَّا يَطْعَمُهَآ إِلَّا مَن
نَّشَآءُ بِزَعْمِهِمْ وَأَنْعَٰمٌ حُرِّمَتْ ظُهُورُهَا وَأَنْعَٰمٌ
لَّا يَذْكُرُونَ اَسْمَ اَللَّهِ عَلَيْهَا اَفْتِرَآءً عَلَيْهِ سَيَجْزِيهِم بِمَا
كَانُواْ يَفْتَرُونَ ﴿139﴾ وَقَالُواْ مَا فِي بُطُونِ هَٰذِهِ اِلْأَنْعَٰمِ
خَالِصَةٌ لِّذُكُورِنَا وَمُحَرَّمٌ عَلَىٰٓ أَزْوَٰجِنَا وَإِن يَكُن
مَيْتَةً فَهُمْ فِيهِ شُرَكَآءُ سَيَجْزِيهِمْ وَصْفَهُمْ إِنَّهُۥ
حَكِيمٌ عَلِيمٌ ﴿140﴾ قَدْ خَسِرَ اَلَّذِينَ قَتَلُواْ أَوْلَٰدَهُمْ
سَفَهًا بِغَيْرِ عِلْمٍ وَحَرَّمُواْ مَا رَزَقَهُمُ اُللَّهُ اُفْتِرَآءً
عَلَى اَللَّهِ قَدْ ضَلُّواْ وَمَا كَانُواْ مُهْتَدِينَ ﴿141﴾
۞ وَهُوَ اَلَّذِيٓ أَنشَأَ جَنَّٰتٍ مَّعْرُوشَٰتٍ وَغَيْرَ مَعْرُوشَٰتٍ
وَالنَّخْلَ وَالزَّرْعَ مُخْتَلِفًا اُكُلُهُۥ وَالزَّيْتُونَ وَالرُّمَّانَ
مُتَشَٰبِهًا وَغَيْرَ مُتَشَٰبِهٍ كُلُواْ مِن ثَمَرِهِۦٓ إِذَآ أَثْمَرَ
وَءَاتُواْ حَقَّهُۥ يَوْمَ حِصَادِهِۦ وَلَا تُسْرِفُوٓاْ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ اُلْمُسْرِفِينَ ﴿142﴾
وَمِنَ اَلْأَنْعَٰمِ حَمُولَةً وَفَرْشًا كُلُواْ مِمَّا رَزَقَكُمُ اُللَّهُ
وَلَا تَتَّبِعُواْ خُطُوَٰتِ اِلشَّيْطَٰنِ إِنَّهُۥ لَكُمْ عَدُوٌّ مُّبِينٌ ﴿143﴾

ربع

139. Sukace, "Wađannan dabbobi da hatsi, haramun ne ba mai taɓa su sai wanda muka ga dama (na daga masuyiwa gu-maka hidima da waninsu) a riyawarsu (basu da hujja a cikin wannan,) da dabbobi da aka haramta bayanta (baza a hau ta ba, kamar bayan gumaka da iya yen maza na gumaka) da dabbobi da ba a ambato sunan Allah yayin (yankanta sai sunan gumaka, suka kuma dangana wannan izuwa Allah) don ƙage a gareshi. Da sannu zai saka musu abinda suke ƙirƙiran (nan a gareshi).

140. Sukace, "Abinda yake cikin cikkunan wađannan dabbobi (abar haramtawar bayan gunki da uban maza,) halal ne ga mazajenmu haram ne ga matayenmu. Idan ya zama mushe su masu tarayya ne a cikin sa". Da sannu Allah zai sakamusu wannan sufantawarsu (na halacci da haramci). Ubangiji gwanine (cikin aikinsa) masanine da (halittarsa).

141. Haƙiƙa wađanda suka binne "ya" yansu da rai (ko suka sha ƙwayoyi don rage haihuwa) don wauta ba tareda wani ilimi basun taɓe, sun haramta abinda Allah ya azurta musu (na daga abinda aka ambata) don girba ƙarya bisa Allah. Haƙiƙa sun ɓata, basu kasance masu shiriya ba. (Allah ya kiyashemu, Amin).

(WANI ABU DAGA MANA KAN IKON ALLAH DA NI'IMOMINSA DA RADDI A KAN MUSHIRIKAI)

142. Shine wanda ya halicci gona-kai (wato tsirrai,) ababen shimfiđawa (wato masu kwanciya a ƙas) da wasunsu (kamar kankana da wasunsu kamar dabinai) kuma (ya halicci) dabinai da hatsaitsai mai sassaɓawar "ya" ya da ƙwaya a kama da đanđano, da zaitun da rumman mai kama da juna (a wajen ganyensa) mai kama (a cikin đanđaninsaba). Kuci daga "ya" yan itaciyarsa idan yayi "ya" ya (kafin ya nuna,) ku bada zakkarsa zamanin da ƙitar da zakkarsa ta sawwaƙa. Kada kuyi barna (ku bayar dashi dukkansa baku wanzar da komai ba ga iyalinku). Haƙiƙa al'amarin, Allah ba yason masu shisshigi.

143. Ya halitta daga dabbobi mai kyautuwa ga đaukar kaya (kamar manyan raƙumai) da wađanda basu ingantada đora kaya a kansu (kamar kananan raƙuma da tumakai,) Kuci daga abinda Allah ya azurta muku, kadaku ,bi hanyoyin shaiđan (a cikin haramci da halacci). Shi (shaiđan) haƙiƙa magauci ne mabayyanin ƙiyayya a gareku.

ثَمَٰنِيَةَ أَزْوَٰجٍ مِّنَ اَ۬لضَّأْنِ اِ۪ثْنَيْنِ وَمِنَ اَ۬لْمَعْزِ اِ۪ثْنَيْنِۖ
قُلْ ءَآلذَّكَرَيْنِ حَرَّمَ أَمِ اِ۬لْأُنثَيَيْنِ أَمَّا اَ۪شْتَمَلَتْ عَلَيْهِ
أَرْحَامُ اُ۬لْأُنثَيَيْنِۖ نَبِّـُٔونِے بِعِلْمٍ اِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَۖ 144
وَمِنَ اَ۬لْإِبِلِ اِ۪ثْنَيْنِ وَمِنَ اَ۬لْبَقَرِ اِ۪ثْنَيْنِۖ قُلْ
ءَآلذَّكَرَيْنِ حَرَّمَ أَمِ اِ۬لْأُنثَيَيْنِ أَمَّا اَ۪شْتَمَلَتْ عَلَيْهِ
أَرْحَامُ اُ۬لْأُنثَيَيْنِۖ أَمْ كُنتُمْ شُهَدَآءَ اِذْ وَصَّيٰكُمُ اُ۬للَّهُ بِهَٰذَاۖ
فَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ اِ۪فْتَرَيٰ عَلَى اَ۬للَّهِ كَذِباً لِّيُضِلَّ
اَ۬لنَّاسَ بِغَيْرِ عِلْمٍۖ اِنَّ اَ۬للَّهَ لَا يَهْدِے اِ۬لْقَوْمَ اَ۬لظَّٰلِمِينَۖ 145
* قُل لَّآ أَجِدُ فِے مَآ أُوحِيَ إِلَيَّ مُحَرَّماً عَلَيٰ طَاعِمٖ يَطْعَمُهُۥٓ
إِلَّآ أَن يَكُونَ مَيْتَةً اَوْ دَماً مَّسْفُوحاً اَوْ لَحْمَ خِنزِيرٖ
فَإِنَّهُۥ رِجْسٌ اَوْ فِسْقاً اُهِلَّ لِغَيْرِ اِ۬للَّهِ بِهِۦۖ فَمَنُ اُ۟ضْطُرَّ
غَيْرَ بَاغٖ وَلَا عَادٖ فَإِنَّ رَبَّكَ غَفُورٞ رَّحِيمٞۖ 146
وَعَلَى اَ۬لَّذِينَ هَادُواْ حَرَّمْنَا كُلَّ ذِے ظُفُرٖۖ وَمِنَ اَ۬لْبَقَرِ وَالْغَنَمِ
حَرَّمْنَا عَلَيْهِمْ شُحُومَهُمَا إِلَّا مَا حَمَلَتْ ظُهُورُهُمَا أَوِ اِ۬لْحَوَايَا
أَوْ مَا اَ۟خْتَلَطَ بِعَظْمٖۖ ذَٰلِكَ جَزَيْنَٰهُم بِبَغْيِهِمْۖ وَإِنَّا لَصَٰدِقُونَۖ 147

ثمن

144. Nau'i takwas daga tumakai aure biyu; namiji da mace, da awaki aure biyu. Cene (ga wanda ya haramta mazajen dabbobi ya ambatada haramta matayenta wani Lokaci ya dangana wannan izuwa Allah, cene,) "Shin mazajen tumakai da awakai su Allah ya haramta (a gareku) ko kuwa matayen (daga cikinsu,) ko abinda mahaifar matayen nan guda biyu suka tattarar (a kansa namiji ko mace?) ku bani Labari da ilimi ga kaifiyar haramcin wannan, in kun kasance magaskata.

145. Daga raƙuma biyu daga shanu biyu, Cene, "Mazajen aka haramta ko matayen? ko kuna nan ne mahalarta zamanin da Allah yayi muku wasiyya da wannan (haramcin?) To. babu mafi zalunci daga wanda ya ƙirƙiri ƙarya bisa Ubangiji donya ɓatar da mutane bada ilimi ba. Haƙiƙa Ubangiji baya shiriyar mutane kafirai.

(ABINDA ALƘUR'ANI YA HARAMTADA ABINDA ATTAURA TA HARAMTA NA DAGA DANGOGIN ABINCI)

146. Cene "Bana samu daga abinda aka aiko gare ni abin haramtawa a bisa mai ɗanɗanon dazai ɗanɗane shi, sai ko in ya zama mushe ne, ko jini abin zubarwa,(jinin - ha da - hu wato wanda yake shiga cikin dabbada wanda yake fitowa tada ga jinkinta, ban da hanta ban da saifa) ko naman alhinzir, to haƙiƙa shi haramun ne, ko in ya zama fasiƙanci (wato wanda aka ambaci sunan wanin Allah a wurin yankansa. To, wanda aka tilastar dashi izuwa abinda aka ambata din nan, yaci shi ba yana ɗan tawaye ba, ba mai shisshigi ba, to, haƙiƙa Ubangijin ka mai gafara ne mai jinƙai (dashi. Tsuntsaye a wurin Imam Maliku duk halal ne sai jemage, duk namun jeji makaruhai ne sai karen gida da biri. Amma doki da alfadari da jakin gida to haramun ne a mashahurin mazhabin Iman maliki. Shafi'i kuma ya halatta cin doki ban da alfadari da jaki).

147. Mun haramta dukkan mai kofato a bisa Yahudawa (wato shine wanda "yanyatsunsa basu rabu ba) daga shanu da tumakai, mun haramta musu kitsen (amma naman halal ne garesu) sai abinda ya ɗamfara da bayansu ko kayan ciki (wato irin kitsutsuwan dasuke tareda kayan ciki, to wannan shi an halatta musu) ko abinda ya cudanyu da kashi (wato kamar ɗuwawu.) Wancananaka (haramci) mun saka musu dashi saboda zaluncin (da suka gabatar dashi.) Mu haƙiƙa magaskata ne mu a (cikin labarinmu.).

(TAUSASAWA A CIKIN KIRA IZUWA IMANI)

فَإِن كَذَّبُوكَ فَقُل رَّبُّكُمْ ذُو رَحْمَةٍ وَاسِعَةٍ وَلَا يُرَدُّ بَأْسُهُۥ
عَنِ الْقَوْمِ الْمُجْرِمِينَ ﴿148﴾ سَيَقُولُ الَّذِينَ أَشْرَكُواْ لَوْ شَآءَ اللَّهُ
مَا أَشْرَكْنَا وَلَا ءَابَآؤُنَا وَلَا حَرَّمْنَا مِن شَيْءٍ كَذَٰلِكَ كَذَّبَ
الَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ حَتَّىٰ ذَاقُواْ بَأْسَنَا قُلْ هَلْ عِندَكُم مِّنْ عِلْمٍ
فَتُخْرِجُوهُ لَنَا إِن تَتَّبِعُونَ إِلَّا الظَّنَّ وَإِنْ أَنتُمْ إِلَّا تَخْرُصُونَ ﴿149﴾
قُلْ فَلِلَّهِ الْحُجَّةُ الْبَالِغَةُ فَلَوْ شَآءَ لَهَدَىٰكُمْ أَجْمَعِينَ ﴿150﴾
قُلْ هَلُمَّ شُهَدَآءَكُمُ الَّذِينَ يَشْهَدُونَ أَنَّ اللَّهَ
حَرَّمَ هَٰذَا فَإِن شَهِدُواْ فَلَا تَشْهَدْ مَعَهُمْ وَلَا تَتَّبِعْ
أَهْوَآءَ الَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَالَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ
بِالْأٓخِرَةِ وَهُم بِرَبِّهِمْ يَعْدِلُونَ ﴿151﴾ * قُلْ تَعَالَوْاْ أَتْلُ مَا حَرَّمَ
رَبُّكُمْ عَلَيْكُمْ أَلَّا تُشْرِكُواْ بِهِۦ شَيْـًٔا وَبِالْوَٰلِدَيْنِ
إِحْسَٰنًا وَلَا تَقْتُلُواْ أَوْلَٰدَكُم مِّنْ إِمْلَٰقٍ نَّحْنُ
نَرْزُقُكُمْ وَإِيَّاهُمْ وَلَا تَقْرَبُواْ الْفَوَٰحِشَ مَا ظَهَرَ
مِنْهَا وَمَا بَطَنَ وَلَا تَقْتُلُواْ النَّفْسَ الَّتِي حَرَّمَ اللَّهُ
إِلَّا بِالْحَقِّ ذَٰلِكُمْ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿152﴾

ربع

148. To, idan basu gaskata ka ba a cikin abinda ka zo dashi, cene dasu "Ubangijinka mai rahama ne mayalwaci ya saboda bai yi muku gaggawa da uƙuba ba Ba a mayar da azabarsa ga buran mutane ma'abuta Laifi".

(SHUBUHA RARRAUNA WATO HANZARINKARYA) (1)

149. Da sannu waɗanda suke mushirikai zasu dinga cewa "Da Allah yaga dama da bazamuyi shirka ba wala iyayenmu, bazamu haramta wani abu ba, (to, ashe Allah ne yanufi haka. To ashe ya yarda dashi ke nan)".To, sai Ubangiji yace "Tamfar yadda waɗannan suka ƙaryata manzanninsu daga gabansu haka nan waɗanda suke gabansu suka ƙaryata manzanni har muka ɗanɗana musu tsananin azabarmu, wacce suka koɗa tada hannunsu". Cene dasu yalla kuna da wani ilimi ne da cewa Allah ya yarda da wannan? To, ku nuna mana shi, a'a! ba ilimin kome gareku, ba kwa bin kome cikin wannan sai zato, ku baku kasance ba sai masu kuta ƙarya kawai.

150. Cene (dasu in basu da wata hujja) to, Allah yana da hujja cikakkiya. Da Allah yanufi shi-riyarsu daya shirye su. baki daya".

151. Cene "Ku kawo shaidun ku waɗanda suke shaida muku cewa haƙiƙa Allah ne ya haramta muku abin nan da kuke haramtawa, to, in sun shaidar kadaka ƙara halarta tare dasu kadaka ƙara shaida taredasu, kadaka bi son zuciyar waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu, waɗanda basu bada gaskiya da ranar Lahira basu suna shirkantawa da Ubangijinsu".

(ASALAN ABABAN HARAMTAWA DATA DODI NAGARI A CIKIN MUSULUNCI WAƊANDASUNE SHARUDDAN KOWACE DARIKA TA MUSULUNCI TAFSILAN)

152. Cene, "Kuzo in karanta abinda Ubangijinku ya haramta a gareku, kadaku, shirkanta kome da Allah, ku kyautata ga iyaye kyautatawa, kadaku ,binne "ya" yankuda rai saboda gudun talauci, (wanda ke shan ƙwayoyi don rage haihuwa yana daga ciki) Mune muke azurta ku taredasu, kadaku ,kusanci aikin alfasha da kaba'ira, (ta kai wajen dari bakwai kamar yadda Ibn Hujjurim ya fada a cikin Littafinsa Zawajuru) abinda ya bayyana daga garetada abinda ya ɓuya. Kadaku ,kashe kai wacce Allah ya haramta ta saida gaskiya, (kamar ƙisasi da haddin ridda da rajamu na katangantacce). Wancananku abin ambato Allah yayi muku wasiyya dashi don kuyi Lura.

1) Mutumne wanda yafita neman abinci tun safe bai dawo ba sai dare amma bai kawo komai ba sai barkono.

وَلَا تَقْرَبُواْ مَالَ اَ۬لْيَتِيمِ إِلَّا بِالتِي هِيَ أَحْسَنُ حَتَّىٰ يَبْلُغَ
أَشُدَّهُۥ وَأَوْفُواْ اُ۬لْكَيْلَ وَالْمِيزَانَ بِالْقِسْطِ لَا نُكَلِّفُ
نَفْساً اِلَّا وُسْعَهَا وَإِذَا قُلْتُمْ فَاعْدِلُواْ وَلَوْ كَانَ
ذَا قُرْبَىٰ وَبِعَهْدِ اِ۬للَّهِ أَوْفُواْ ذَٰلِكُمْ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمْ
تَذَّكَّرُونَ (153) وَأَنَّ هَٰذَا صِرَٰطِي مُسْتَقِيماً فَاتَّبِعُوهُ
وَلَا تَتَّبِعُواْ اُ۬لسُّبُلَ فَتَفَرَّقَ بِكُمْ عَن سَبِيلِهِۦ ذَٰلِكُمْ وَصَّىٰكُم بِهِۦ
لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ (154) ثُمَّ ءَاتَيْنَا مُوسَى اَ۬لْكِتَٰبَ تَمَاماً عَلَى اَ۬لذِي
أَحْسَنَ وَتَفْصِيلاً لِّكُلِّ شَيْءٍ وَهُدىً وَرَحْمَةً لَّعَلَّهُم بِلِقَآءِ
رَبِّهِمْ يُؤْمِنُونَ (155) وَهَٰذَا كِتَٰبٌ اَنزَلْنَٰهُ مُبَٰرَكٌ فَاتَّبِعُوهُ وَاتَّقُواْ
لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ (156) أَن تَقُولُواْ إِنَّمَا أُنزِلَ اَ۬لْكِتَٰبُ عَلَىٰ
طَآئِفَتَيْنِ مِن قَبْلِنَا وَإِن كُنَّا عَن دِرَاسَتِهِمْ لَغَٰفِلِينَ (157)
أَوْ تَقُولُواْ لَوَ اَنَّآ أُنزِلَ عَلَيْنَا اَ۬لْكِتَٰبُ لَكُنَّا أَهْدَىٰ مِنْهُمْ فَقَدْ
جَآءَكُم بَيِّنَةٌ مِّن رَّبِّكُمْ وَهُدىً وَرَحْمَةٌ فَمَنْ أَظْلَمُ
مِمَّن كَذَّبَ بِـَٔايَٰتِ اِ۬للَّهِ وَصَدَفَ عَنْهَا سَنَجْزِي اِ۬لذِينَ
يَصْدِفُونَ عَنْ ءَايَٰتِنَا سُوٓءَ اَ۬لْعَذَابِ بِمَا كَانُواْ يَصْدِفُونَ (158)

153. Kadaku ,kusanci dukiyar maraya, saida ta'ada da take mafi kyau, (wato abinda gyara yake ciki,) har saiya isa hankalinsa (shine ya balaga). Ku cika mudu da ma'auni da adalci, Barna kallafawa kowa sai gwargwadon ikonsa. Idan zakuyi magana (cikin hukunci ko waninsa) kuyi adalci da gaskiya, koda wandaza ayi wa hukuncin (mai dađi ne ko mara dađi gareshi) ko đan' uwa ne na zu-munci. Ku cika alƙawarin Allah, wancananka ku Allah yayi muku wasiyya dashi don ku gargađu.

154. Cewa haƙiƙa wannan wasiyya hanyata ke nan madaidaiciya, kubi ta, ka daku ,bi hanyoyi wađanda suka saɓa mata sai, ta rarrabadaku ,ga buran Addinin Allah. Wancananku Allah yayi muku wasiyya dashi don kuji tsoronsa.

(ALƘUR'ANI TAREDA WANDA YAGASKATA SHI DA WANDA YA KAFIRTA DASHI)

155. Sannan muka baiwa Annabi Musa (Alaihissalam) Attaura don cikawa (ga ni'ima) a kan wanda ya kyautata aiki (daga cikinsu,) da rarrabewa ga dukkan abin (da ake bukata gareshi a cikin addini,) dashirya da rahama ko sa bada gaskiya da saduwa da Ubangijinsu.

156. Wannan Alƙur'ani Littafi ne da muka saukar dashi mai albarka, kubi shi yaku mutanen Makka da aiki da abinda yace cikin sa kuji tsoron Allah don ko kwa sami rahamar Allah

157. (Mun saukar muku dashine) don kadaku ,ce an saukar da Littafi ne a bisa jama'a guda biyu dasuke gabanmu kawai, (Yahudu da Nasara,) mu ko mun kasance marabkana ga buran karatunsu. (Bamu san harshensu ba).

158. Koku ce, "Da an saukar da Littafi gare mu, da mun kasance mafiya shiriya dagasu (saboda kyan hankulanmu). Haƙiƙa bay-ani yazo muku daga Ubangijinku dashiriya da jinƙai (ga wanda yabi shi). Babu mafi zalunci daga wanda ya ƙaryata Ayoyin Allah, ya kangare mata. Da sannu zamu đanđanawa wanđanda suka kangare wa ayoyinmu mummunar azaba, saboda kan-garewarsu.

(FIRGITARWA DA TSORATARWA) WANDA YAKUNSHI HUDOWAR RANA DA WATA DAGA YAMMA

ثمن

* هَلْ يَنظُرُونَ إِلَّآ أَن تَأْتِيَهُمُ الْمَلَٰٓئِكَةُ أَوْ يَأْتِيَ رَبُّكَ أَوْ يَأْتِيَ
بَعْضُ ءَايَٰتِ رَبِّكَ يَوْمَ يَأْتِي بَعْضُ ءَايَٰتِ رَبِّكَ لَا يَنفَعُ
نَفْسًا إِيمَٰنُهَا لَمْ تَكُنْ ءَامَنَتْ مِن قَبْلُ أَوْ كَسَبَتْ فِي إِيمَٰنِهَا
خَيْرًا قُلِ انتَظِرُوا إِنَّا مُنتَظِرُونَ (159) إِنَّ الَّذِينَ فَرَّقُوا دِينَهُمْ
وَكَانُوا شِيَعًا لَّسْتَ مِنْهُمْ فِي شَيْءٍ إِنَّمَا أَمْرُهُمْ إِلَى اللَّهِ ثُمَّ يُنَبِّئُهُم
بِمَا كَانُوا يَفْعَلُونَ (160) مَن جَآءَ بِالْحَسَنَةِ فَلَهُ عَشْرُ أَمْثَالِهَا
وَمَن جَآءَ بِالسَّيِّئَةِ فَلَا يُجْزَىٰ إِلَّا مِثْلَهَا وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ (161) قُلْ
إِنَّنِي هَدَىٰنِي رَبِّي إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ (162) دِينًا قِيَمًا مِّلَّةَ إِبْرَٰهِيمَ حَنِيفًا
وَمَا كَانَ مِنَ الْمُشْرِكِينَ (163) قُلْ إِنَّ صَلَاتِي وَنُسُكِي وَمَحْيَايْ وَمَمَاتِي
لِلَّهِ رَبِّ الْعَٰلَمِينَ (164) لَا شَرِيكَ لَهُ وَبِذَٰلِكَ أُمِرْتُ وَأَنَا أَوَّلُ الْمُسْلِمِينَ (165)
قُلْ أَغَيْرَ اللَّهِ أَبْغِي رَبًّا وَهُوَ رَبُّ كُلِّ شَيْءٍ وَلَا تَكْسِبُ كُلُّ نَفْسٍ
إِلَّا عَلَيْهَا وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٌ وِزْرَ أُخْرَىٰ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُم مَّرْجِعُكُمْ
فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ فِيهِ تَخْتَلِفُونَ (166) وَهُوَ الَّذِي جَعَلَكُمْ خَلَٰٓئِفَ
الْأَرْضِ وَرَفَعَ بَعْضَكُمْ فَوْقَ بَعْضٍ دَرَجَٰتٍ لِّيَبْلُوَكُمْ
فِي مَآ ءَاتَىٰكُمْ إِنَّ رَبَّكَ سَرِيعُ الْعِقَابِ وَإِنَّهُ لَغَفُورٌ رَّحِيمٌ (167)

159. Masu ƙaryatawar Alƙur'ani basa sauraren komai sai Mala'iku sun zo don karɓar rayukansu ko kuma Ubangijinka yazo (wato azabarsa) ko ba'alin ayoyin Ubangijinka (wato alamomi masu shiryarwa bisa tashin alƙiyama) ranar da ba'alin ayoyin Ubangijinka zaizo (shine hudowar rana daga yamma) imanin wata kai bazai anfane ta ba; wacce bata kasance ta bada gaskiya tun kafin zuwan ayar ba, ko bata kasance ta aikata alheri a cikin imanin nata ba, (wato in ta tuba a wannan rana baza a karɓa ba). Cene, "Ku saurari (ɗayan waɗannan abubu-wa) ni ma ina sauraro. kamar da hadisi yace:

(AƘIBAR SABANI DA RASHIN HADA KAI)

160. Waɗannan da suka rarraba addininsu (suka sassaba a cikinsa, suka aikata ba'ali suka bar ba'ali) suka zama daban - daban (wato sune Yahudu da Nasara), baka cikin kome daga garesu (wato ba ruwan ka dasu). Al'amarinsu kawai yana ga Allah, sannan Ranar Lahira Allah zai saka musu abinda suka aikata. (to muma fa al'ummar Annabi alaihissalam ɗaya muke a wannan. aya in mukayi yadda suka yi).

(FALALAR LA'ILAHA ILLALLAHU DA MAKAMANTANTA)

161. Wanda yazoda 'Hasana'(iTace La'ilaha Illallahu) to yana da goma ɗin tamkanninta (wato yana da lada goma). Wanda yazoda mummunan aiki to, baza a saka masa ba saitankarsa, su baza a zalunce su komai ba.

(TAUHIDI DA IHLASI A CIKIN KUDURI DA AIKI DA SAKAMAKO A KANSAI

162. Cene, "Haƙiƙa ni Ubangijina ya shirye ni izuwa tafarki madaidaici".
163. "Addinin kyam, Addinin Annabi Ibrahima (Alaihissalam) totar, bai kasance daga mushirikai ba".
164. Cene, "Haƙiƙa sallatada ibadatada hajji da waninsa da rayuwatada mutuwata ta Allah ce Ubangijin talikai.
165. "Bashi da abokin tarayya. Da wannan tauhidi kaɗai aka umarce ni. Nine farkon Musulmi (daga cikin wannan al'umma)".
166. Cene, "Shin wanin Allah zan nema Ubangiji. alhali shine Ubangijin komai! Kowace kai bazata tsuwurwurta ba sai a kanta, wata kai bazata ɗauki zunubin wata kai ba, sannan izuwa Ubangijinku za a koma daku ,ya ɗanɗana muku kudarku a cikin abinda kuka kasance kuna saɓawa a cikinsa".

(AL'ADAR ALLAH A CIKIN HALITTA)

167. Shine wanda yasanya ku masu mayewa a bayan ƙasa, (wannan ya maye wannan,) Ya ɗaukaka ba'alinku a kan ha'ali a darajoji, (ilmi, dukiya, alfarma, da waninsa) donya jarrabe ku a cikin abinda ya baku, yaga mai bi da mai taurin kai. Haƙiƙa Ubangijinka mai gaggawar uƙubane (ga wanda ya saɓe shi). Haƙiƙa shi mai gafara ne (ga muminai) mai jinƙai (dasu).

ANBUGA ITA WANNA ALƘUR'ANI MAI GIRMA KEWTA DAGA T MUSLIMJI TRABLUS - JAMAHIRH

حزب

7 سُورَةُ الأعراف مَكِّيَّة

وهي مائتان وست آيات 206

بِسْمِ اِ۬للَّهِ اِ۬لرَّحْمَٰنِ اِ۬لرَّحِيمِ

* الٓمٓصٓ كِتَٰبٌ اُنزِلَ إِلَيْكَ فَلَا يَكُن فِے صَدْرِكَ حَرَجٞ مِّنْهُ لِتُنذِرَ بِهِۦ
وَذِكْرَىٰ لِلْمُؤْمِنِينَ (1) اِتَّبِعُواْ مَا أُنزِلَ إِلَيْكُم مِّن رَّبِّكُمْ وَلَا تَتَّبِعُواْ مِن
دُونِهِۦٓ أَوْلِيَآءَ قَلِيلاٗ مَّا تَذَّكَّرُونَ (2) وَكَم مِّن قَرْيَةٍ اَهْلَكْنَٰهَا
فَجَآءَهَا بَأْسُنَا بَيَٰتاً اَوْ هُمْ قَآئِلُونَ (3) فَمَا كَانَ دَعْوَيٰهُمْ
إِذْ جَآءَهُم بَأْسُنَا إِلَّا أَن قَالُواْ إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ (4) فَلَنَسْـَٔلَنَّ
اَ۬لذِينَ اُرْسِلَ إِلَيْهِمْ وَلَنَسْـَٔلَنَّ اَ۬لْمُرْسَلِينَ (5) فَلَنَقُصَّنَّ عَلَيْهِم
بِعِلْمٍ وَمَا كُنَّا غَآئِبِينَ (6) وَالْوَزْنُ يَوْمَئِذٍ اِ۬لْحَقُّ فَمَن ثَقُلَتْ
مَوَٰزِينُهُۥ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ اُ۬لْمُفْلِحُونَ (7) وَمَنْ خَفَّتْ مَوَٰزِينُهُۥ فَأُوْلَٰٓئِكَ
اَ۬لذِينَ خَسِرُواْ أَنفُسَهُم بِمَا كَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يَظْلِمُونَ (8)
وَلَقَدْ مَكَّنَّٰكُمْ فِے اِ۬لْأَرْضِ وَجَعَلْنَا لَكُمْ فِيهَا مَعَٰيِشَ قَلِيلاٗ
مَّا تَشْكُرُونَ (9) وَلَقَدْ خَلَقْنَٰكُمْ ثُمَّ صَوَّرْنَٰكُمْ ثُمَّ قُلْنَا لِلْمَلَٰٓئِكَةِ
اِ۟سْجُدُواْ لِأدَمَ فَسَجَدُوٓاْ إِلَّا إِبْلِيسَ لَمْ يَكُن مِّنَ اَ۬لسَّٰجِدِينَ (10)

Suratul A'arafi

A Makka Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Metan Dashida (206)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabaɗaya, mai jinƙan Muittinai a Lahira a keɓe

(KIRARI GA ALƘUR'ANI DA UMARNI A BISA BIN SA)

1. Alif - Lam - Mim - Sad, Allah ne yasan abinda Yake nufi da wannan kalma (Wannan) littafi ne da aka saukar izuwa gareka (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama). Kada ƙunci ya samu a kirjinka daga gareshi. (An saukar dashi) don kayi gargadi dashi kayi wa'azi ga muminai.
2. (Cene dasu) "Kubi abinda aka saukar "izuwa gareku daga Ubangijinku (Alƙur'ani) kadaku ,bi (shiyagabanni ko kuma iyayen ɗaki da zakubi su cikin saɓon Allah) ba Allah ba. Kaɗan ne ƙwarai kuke wa'azantuwa.

(AƘIBAR SABO A DUNIYA)

3. Da yawa daga mutanen alƙarya muka nufi halakar dasu, azabarmu tazo musu da dare, ko da rana suna ƙailula (wato barcin rana saboda hutawa).
4. Basu ce komi bazamanin da azabarmu tazo musu, sai kawai cewa "Mu mun kasance azzalumai".

(AƘIBAR KAFIRCI DA FASIƘANCI A LAHIRA)

5. Lalle zamu tambayi waɗanda aka aiko daga cikinsu (na daga al'umma ko sun amsawa manzanni?) Lalle zamu tambayi manzanni shin (sun iyar?).
6. To, Lalle zamu Labarta musu da ilimi (da abinda suka aikata, wato zasu ɗanɗana kuɗarsu). Bamu kasance marabkana ba (ga buran iyarwar manzanni da al'umma data wuce cikin abinda suka aikata).

(AUNA AIYYUKA)

7. Auna aiki a wannan rana gaskiya ne, to, wanda ma'aunansa sukayi nauyi (da aiki nagari,) to, waɗannan sune marabauta.
8. Wanda ma'aunansa sukayi shafal (da aiki mummuna,) to. waɗancananka sune waɗanda suka taɓar da kawukansu (saboda makomarsu Jahannama) Don sun , kasance suna musun ayoyinmu.

(NI'IMOMIN ALLAH A BISA MUTANE)

9. Haƙiƙa mun.tabbatar daku ,(Yaku Bani -Adamu) a cikin ƙasa, mun sanya muku rayuwa a cikinta, kaɗan ne ƙwarai kuke godewa (Allah).

(GIRMAMA ' YAN - ADAM DA MATSAYIN IBLIS DAGA GARESU)

10. Haƙiƙa mun halicce ku (uban ku Adamu) sannan muka suranta ku (a cikin bayansa,) sannan mukace da Mala'iku "Kuyi sujjada ga Annabi Adamu (Alaihissalam, sunkuya wuya don gaisuwa) sukayi sujada sai Iblis kaɗai (uban aljannu yana tsakanin Mala'iku) bai kasance cikin masu sujada ba.

قَالَ مَا مَنَعَكَ أَلَّا تَسْجُدَ إِذْ أَمَرْتُكَ قَالَ أَنَا خَيْرٌ مِّنْهُ خَلَقْتَنِي مِن نَّارٍ
وَخَلَقْتَهُ مِن طِينٍ ﴿11﴾ قَالَ فَاهْبِطْ مِنْهَا فَمَا يَكُونُ لَكَ أَن
تَتَكَبَّرَ فِيهَا فَاخْرُجْ إِنَّكَ مِنَ الصَّاغِرِينَ ﴿12﴾ قَالَ أَنظِرْنِي إِلَىٰ
يَوْمِ يُبْعَثُونَ ﴿13﴾ قَالَ إِنَّكَ مِنَ الْمُنظَرِينَ ﴿14﴾ قَالَ فَبِمَا أَغْوَيْتَنِي
لَأَقْعُدَنَّ لَهُمْ صِرَاطَكَ الْمُسْتَقِيمَ ﴿15﴾ ثُمَّ لَآتِيَنَّهُم مِّنۢ بَيْنِ أَيْدِيهِمْ
وَمِنْ خَلْفِهِمْ وَعَنْ أَيْمَانِهِمْ وَعَن شَمَآئِلِهِمْ وَلَا تَجِدُ أَكْثَرَهُمْ
شَاكِرِينَ ﴿16﴾ قَالَ اخْرُجْ مِنْهَا مَذْءُومًا مَّدْحُورًا لَّمَن تَبِعَكَ
مِنْهُمْ لَأَمْلَأَنَّ جَهَنَّمَ مِنكُمْ أَجْمَعِينَ ﴿17﴾ * وَيَا آدَمُ اسْكُنْ أَنتَ ثمن
وَزَوْجُكَ الْجَنَّةَ فَكُلَا مِنْ حَيْثُ شِئْتُمَا وَلَا تَقْرَبَا هَٰذِهِ الشَّجَرَةَ
فَتَكُونَا مِنَ الظَّالِمِينَ ﴿18﴾ فَوَسْوَسَ لَهُمَا الشَّيْطَانُ لِيُبْدِيَ لَهُمَا
مَا وُورِيَ عَنْهُمَا مِن سَوْآتِهِمَا وَقَالَ مَا نَهَاكُمَا رَبُّكُمَا عَنْ هَٰذِهِ الشَّجَرَةِ
إِلَّا أَن تَكُونَا مَلَكَيْنِ أَوْ تَكُونَا مِنَ الْخَالِدِينَ ﴿19﴾ وَقَاسَمَهُمَا إِنِّي لَكُمَا لَمِنَ
النَّاصِحِينَ ﴿20﴾ فَدَلَّاهُمَا بِغُرُورٍ فَلَمَّا ذَاقَا الشَّجَرَةَ بَدَتْ لَهُمَا سَوْآتُهُمَا
وَطَفِقَا يَخْصِفَانِ عَلَيْهِمَا مِن وَرَقِ الْجَنَّةِ وَنَادَاهُمَا رَبُّهُمَا أَلَمْ أَنْهَكُمَا
عَن تِلْكُمَا الشَّجَرَةِ وَأَقُل لَّكُمَا إِنَّ الشَّيْطَانَ لَكُمَا عَدُوٌّ مُّبِينٌ ﴿21﴾

11. Ubangiji yace dashi "Me ya hanaka kayi sujada (L, sila ce) zamanin dana umarce ka! Sai yace "Ni na fi shi, ka halicce ni daga wuta ka halicce shi daga taƃo".
12. Yace, "To fita daga Aljanna, bazai yiwu gareka kayi girman kai a cikinta ba, fita! haƙiƙa kai kana cikin wulaƙantattu".
13. Yace, "Saurara min izuwa ranar daza a tashe su".
14. yace, "Haƙiƙa kai kana cikin ababen saurarawa (izuwa busar farko)".
15. yace, "Saboda ka halakar da ni, Lalle zan datse musu hanyar ka madaidaiciya.
16. "Kuma Lalle zan zo musu ta gabansu data bayansu, data damansu, da hagunsu, (Ibni Abbas yace Allah bazai sa ya sami damar zuwa ta saman su ba don kada ya tsare tsakanin bawa da rahamar Allah). Bazaka sami yawaicinsu masu godiya ba".
17. Yace, "Fita daga gareta, wulakantacce tsinanne, lalle wanda yabika daga cikin su zan cika Jahannama daku ,taf! gabaɗaya".

(ƘISSAR ZAMAN ANNABI ADAMU A CIKIN ALJANNA DA FITOWARSA DAGA CIKINTA) WACCE TA ƘUNS - HI SHU'UMIN MA'ASIYA DA RUFIN ASIRIN ALLAH YANA TAREDA DA'A

18. Ubangiji yace, "Ya Adamu zauna kai da matar ka (Hauwa'u) a cikin aljanna. Kuci daga inda kuka ga dama, amma kadaku ,kusanci wannan itaciya (alkama) da ci kwa zama daga azzalumai".
19. Sai shaiɗan yayi musu wuswasi, donya bayyana garesu abinda aka ɓoye ga buransu, na daga tsiraicin su. Yace dasu "Ubangijinku bai hana ku cin wannan itaciya ba, sai don kadaku ,zama Mala'iku koku zama masu dauwama a cikinta".
20. Ya rantse musu da Allah. haƙiƙa ni ina cikin masuyi muku nasiha.
21. Saiya sauko dasu (ga buran darajarsu) saboda ruɗin dayayi musu. Yayin da suka ɗanɗani itaciyar nan, sai tsiraicinsu ya bayyana garesu, suka haɗu suna bankewa a kansu daga ganyen aljanna. Ubangijinsu ya kira su, yace "Yanzu ban hana ku bane ga buran wancananku itaciya! BAnce daku ,haƙiƙa shaiɗan magauci ne mabayyanin kiyayya a gareku ba?

قَالَا رَبَّنَا ظَلَمْنَا أَنفُسَنَا وَإِن لَّمْ تَغْفِرْ لَنَا وَتَرْحَمْنَا لَنَكُونَنَّ
مِنَ الْخَاسِرِينَ ﴿22﴾ قَالَ اهْبِطُوا بَعْضُكُمْ لِبَعْضٍ عَدُوٌّ وَلَكُمْ
فِي الْأَرْضِ مُسْتَقَرٌّ وَمَتَاعٌ إِلَىٰ حِينٍ ﴿23﴾ قَالَ فِيهَا تَحْيَوْنَ وَفِيهَا
تَمُوتُونَ وَمِنْهَا تُخْرَجُونَ ﴿24﴾ يَا بَنِي آدَمَ قَدْ أَنزَلْنَا عَلَيْكُمْ
لِبَاسًا يُوَارِي سَوْآتِكُمْ وَرِيشًا وَلِبَاسُ التَّقْوَىٰ ذَٰلِكَ خَيْرٌ ذَٰلِكَ مِنْ
آيَاتِ اللَّهِ لَعَلَّهُمْ يَذَّكَّرُونَ ﴿25﴾ يَا بَنِي آدَمَ لَا يَفْتِنَنَّكُمُ الشَّيْطَانُ
كَمَا أَخْرَجَ أَبَوَيْكُم مِّنَ الْجَنَّةِ يَنزِعُ عَنْهُمَا لِبَاسَهُمَا لِيُرِيَهُمَا
سَوْآتِهِمَا إِنَّهُ يَرَاكُمْ هُوَ وَقَبِيلُهُ مِنْ حَيْثُ لَا تَرَوْنَهُمْ
إِنَّا جَعَلْنَا الشَّيَاطِينَ أَوْلِيَاءَ لِلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿26﴾
وَإِذَا فَعَلُوا فَاحِشَةً قَالُوا وَجَدْنَا عَلَيْهَا آبَاءَنَا وَاللَّهُ أَمَرَنَا بِهَا
قُلْ إِنَّ اللَّهَ لَا يَأْمُرُ بِالْفَحْشَاءِ أَتَقُولُونَ عَلَى اللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿27﴾
۞ قُلْ أَمَرَ رَبِّي بِالْقِسْطِ وَأَقِيمُوا وُجُوهَكُمْ عِندَ كُلِّ مَسْجِدٍ رُبع
وَادْعُوهُ مُخْلِصِينَ لَهُ الدِّينَ كَمَا بَدَأَكُمْ تَعُودُونَ فَرِيقًا
هَدَىٰ وَفَرِيقًا حَقَّ عَلَيْهِمُ الضَّلَالَةُ إِنَّهُمُ اتَّخَذُوا الشَّيَاطِينَ
أَوْلِيَاءَ مِن دُونِ اللَّهِ وَيَحْسَبُونَ أَنَّهُم مُّهْتَدُونَ ﴿28﴾

22. Sukace, "Ya Ubangijinmu, mun zalunci kanmu, idan bakayi mana gafara ba, ka jiƙanmu, Lalle zamu kasance daga cikin taɓaɓɓu.

(DUNIYAR WATADA SAURAN TAU-RARI BAZAI YIWU SU ZAUNU BA)

23. Ubangiji yace (dasu) ku sauka kas (Adamu da Hauwa'u da abinda sukaƙunsa na zuriyyarsu) sashin ku maƙiyi ne ga sashi, (wannan ya zalunci wannan). Matabbaci ya tabbata a gareku a cikin ƙasa da jin daɗi izuwa ƙarewar ajalinku a cikin wannan mazauni.

24. ubangiji yace a cikin ƙasa zaku rayu, a cikinta zaku mutu daga gareta kuma za a tashe ku.

(WANI ABU DAGA NI'IMOMIN ALLAH A GAREMU DA RASHIN ZARGIN KYAN KAMA DA KYAN SUTTURA DA RASHIN ZARGIN DAUDA DA KAUSASAWA DA KAKKAUSAR TUFA, ABIN NUFI SHINE KYAKKYAWAR NIYYA)

25. Yaku 'yan Adam haƙiƙa mun sauko da tufa mai suturce tsiraici a garekuda kayan ado, tufar tsoron Allah (wato aiki nagari) shi yafi daga wannan. Wancananka yana daga ayoyin Allah donsu wa'azantu.

(TSORATARWADAGA SHARRIN SHAIƊAN DA MAKIRCINSA)

26. Yaku'yan Adam kada shaiɗan yafitince ku tamfar dayafitar da iyayenku ku Annabi Adamu daga aljanna ya tuɓe musu tufafinsu. Haƙiƙa shi shaiɗan yana ganinku shi da rundunarsa ta inda ba kwa ganinsu, (saboda Laushin jikinsu da rashin Launinsu). Haƙiƙa mu mun sanya shaiɗan iyayen ɗaki ga waɗanda basu bada gaskiya ba.

(SHUBUHOHIN MUSHIRIKAI DA HANZARE – HANZARENSU RAUNANA)

27. Idan suka aikata aikin ashsha (kamar mushirikanci da dawafi a ɗakin Allah tsirara, wai su baza suyi ɗawafi cikin tufafin da sukayi saɓon Allah ciki ba aka hane su ga buran wannan) saisu ce "Mun sami iyayenmune a kanta mukayi koyi dasu a kanta, wai Allah ne ya umarce mu da ita. Cene (dasu) "Hakika Allah baya umarni da aikin ashsha. Donme kuke ƙagawa Allah abinda baku sani ba?"

(WAJABCIN IKHLASI A CIKIN AYYUKA)

28. Cene, "Ubangijina yayi umarnine da adalci, yace, "Ku tsaida fuskokinku don Allah, nan ga kowace sujjada (wato ku tsarkake nufi gareshi ga kowace ibada) ku bauta masa kuna masu tsarkake bauta a gareshi, tamfar yadda ya halicce ku, bakuna komai ba, zaku koma ranar Alƙiyama, (waɗansu jama'a daga gareku ya shiriye su, wadansu jama'ar kuwa ɓata ya tabbata a kansu). Haƙiƙa su sun riƙi shaiɗanu iyayen giji ba Allah ba, suna zaton cewa su haƙiƙa su masu shiriya ne.

(WAJABCIN SUTURCE AL AURA A SALLA DA DAWAFI)

يَٰبَنِيٓ ءَادَمَ خُذُواْ زِينَتَكُمْ عِندَ كُلِّ مَسْجِدٖ وَكُلُواْ وَاشْرَبُواْ
وَلَا تُسْرِفُوٓاْۖ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ الْمُسْرِفِينَۖ (29) قُلْ مَنْ حَرَّمَ زِينَةَ اللَّهِ
الَّتِيٓ أَخْرَجَ لِعِبَادِهِۦ وَالطَّيِّبَٰتِ مِنَ الرِّزْقِۖ قُلْ هِيَ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ
فِي الْحَيَوٰةِ الدُّنْيَا خَالِصَةٌ يَوْمَ الْقِيَٰمَةِۖ كَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ الَايَٰتِ
لِقَوْمٖ يَعْلَمُونَۖ (30) قُلْ إِنَّمَا حَرَّمَ رَبِّيَ الْفَوَٰحِشَ مَا ظَهَرَ مِنْهَا
وَمَا بَطَنَ وَالْإِثْمَ وَالْبَغْيَ بِغَيْرِ الْحَقِّ وَأَن تُشْرِكُواْ بِاللَّهِ
مَا لَمْ يُنَزِّلْ بِهِۦ سُلْطَٰنٗا وَأَن تَقُولُواْ عَلَى اللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَۖ (31)
وَلِكُلِّ أُمَّةٍ أَجَلٞۖ فَإِذَا جَا أَجَلُهُمْ لَا يَسْتَأْخِرُونَ سَاعَةٗۖ وَلَا يَسْتَقْدِمُونَۖ (32)
يَٰبَنِيٓ ءَادَمَ إِمَّا يَأْتِيَنَّكُمْ رُسُلٞ مِّنكُمْ يَقُصُّونَ عَلَيْكُمْ ءَايَٰتِي
فَمَنِ اتَّقَىٰ وَأَصْلَحَ فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَۖ (33) وَالَّذِينَ كَذَّبُواْ
بِـَٔايَٰتِنَا وَاسْتَكْبَرُواْ عَنْهَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ النَّارِ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَۖ (34)
فَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ افْتَرَىٰ عَلَى اللَّهِ كَذِبًا أَوْ كَذَّبَ بِـَٔايَٰتِهِۦۖ
أُوْلَٰٓئِكَ يَنَالُهُمْ نَصِيبُهُم مِّنَ الْكِتَٰبِۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَتْهُمْ رُسُلُنَا
يَتَوَفَّوْنَهُمْ قَالُوٓاْ أَيْنَ مَا كُنتُمْ تَدْعُونَ مِن دُونِ اللَّهِۖ قَالُواْ
ضَلُّواْ عَنَّاۖ وَشَهِدُواْ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ أَنَّهُمْ كَانُواْ كَٰفِرِينَۖ (35)

قَالَ ادْخُلُواْ

29. Yaku'yan Adam ku riƙi adon ku (wato abindazai suturce al'aurar ku) nan ga kowane dawafi, Kuci ku sha abinda kuka ga dama, kada kuyi ɓarna. Haƙiƙa Allah ba yason maɓarnata.
30. Cene (dasu) "Wa ya haramta adon Ubangiji wanda yafitar dashi ga bayi (na daga tufa) da daɗaɗa na arziki? (Cene, "Su sun tabbata ga waɗanda suka bada gaskiya a rayuwar duniya da (istihƙaƙi) matsantsanciyace dasu ranar Alƙiyama. Haka nan muke rarrabe ayoyi ga mutane ma'abutan sani".

(SHARUDAN MUSULMAI BALLANTANA SUFAYE DA KUMA DOKOKIN ZAMANI WAƊANDA BASU DACE DA ALƘUR'ANI BA)

31. Cene (dasu) "Dahir dai Ubangijina ya haramta ayyukan alfasha ne (kamar zina) abinda ya bayyana daga garetada abinda ya ɓuya da saɓoda cin zali ba tareda gaskiya ba, kuma a shirkantada Allah da abinda bai saukar da hujja a kansa ba, kuma a girba wa Allah ƙarya na haramta abinda bai haramta ba, da halatta abinda ya haramta. (Dokokin zamani waɗanda basu dace da alƙur'ani basuna daga ciki).

(KOWACE AL'UMMA TANA DA IYAKA)

32. Idan ajalinsu yazo baza suyi jinkiri (ga buransa ba) sa'a ɗaya, bazasu gaggauta a kansa ba.

(MUHIMMANCIN MANZANNI DA AƘIBAR AIKI DA WAJABCIN WASIDA TSAKANIN MU DA ALLAH YAN BIDI'A SUNYI KUSKURE

33. Yaku "yan Adam idan manzanni daga cikin ku sukazo muku suna bayanin ayoyina a gareku, to, wanda yaji tsoron Allah ya kyautata (aikinsa) to, ba tsoro a garesu baza suyi bakin ciki (a Lahira) ba.
34. Waɗanda suka ƙaryata Ayoyinmu sukayi girman kai garesu to, waɗannan sune "yan wuta, su masu dawwama ne a cikinta.

(AƘIBAR ƘARYAGA ALLAH DA AMBATON TSARMAKATAN RANAR ALƘIYAMA)

35. Babu mafi zalunci daga wanda ya kirkiri ƙarya bisa Allah, (da gangan, shariki ko ɗa gareshi,) ko ya ƙaryata Ayoyin Alƙur'ani. Waɗancananka nasibinsu na Littafi zai samesu (na abinda aka rubuta garesu na arziki da ajali da waninsa a Lauhul -Mahfuzu). Har idan jakadunmu (na mala'iku) sukazo musu, suna karɓar ransu saisu ce (dasu don muzantarwa garesu); ina abinda kuka kasance kuna bautawa ba Allah ba? Saisu ce, "Sun ɓace mana (bamu gansu ba)". Suka shaida a kan kansu yayin mutuwa cewa haƙiƙa su sun kasance kafirai.

ثمن

* قَالَ اَدْخُلُواْ فِےٓ أُمَمٖ قَدْ خَلَتْ مِن قَبْلِكُم مِّنَ اَلْجِنِّ
وَالْإِنسِ فِے اِلنَّارِۖ كُلَّمَا دَخَلَتُ اُمَّةٞ لَّعَنَتُ اُخْتَهَاۖ حَتَّىٰٓ إِذَا
اَدَّارَكُواْ فِيهَا جَمِيعاٗ قَالَتُ اُخْرَىٰهُمْ لِأُولَىٰهُمْ رَبَّنَا هَٰٓؤُلَآءِ
أَضَلُّونَا فَـَٔاتِهِمْ عَذَاباٗ ضِعْفاٗ مِّنَ اَلنَّارِۖ 36 قَالَ لِكُلّٖ ضِعْفٞ
وَلَٰكِن لَّا تَعْلَمُونَۖ 37 وَقَالَتُ اُولَىٰهُمْ لِأُخْرَىٰهُمْ فَمَا كَانَ لَكُمْ
عَلَيْنَا مِن فَضْلٖ فَذُوقُواْ اُلْعَذَابَ بِمَا كُنتُمْ تَكْسِبُونَۖ 38
إِنَّ اَلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَاسْتَكْبَرُواْ عَنْهَا لَا تُفْتَحُ لَهُمُۥٓ أَبْوَٰبُ اُلسَّمَآءِ
وَلَا يَدْخُلُونَ اَلْجَنَّةَ حَتَّىٰ يَلِجَ اَلْجَمَلُ فِے سَمِّ اِلْخِيَاطِۖ وَكَذَٰلِكَ
نَجْزِے اِلْمُجْرِمِينَۖ 39 لَهُم مِّن جَهَنَّمَ مِهَادٞ وَمِن فَوْقِهِمْ غَوَاشٖۖ
وَكَذَٰلِكَ نَجْزِے اِلظَّٰلِمِينَۖ 40 وَالَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ اُلصَّٰلِحَٰتِ
لَا نُكَلِّفُ نَفْساً اِلَّا وُسْعَهَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ اُلْجَنَّةِۖ هُمْ فِيهَا
خَٰلِدُونَۖ 41 وَنَزَعْنَا مَا فِے صُدُورِهِم مِّنْ غِلّٖ تَجْرِے مِن
تَحْتِهِمُ اُلْأَنْهَٰرُۖ وَقَالُواْ اُلْحَمْدُ لِلَّهِ اِلَّذِے هَدَىٰنَا لِهَٰذَاۖ وَمَا كُنَّا
لِنَهْتَدِيَ لَوْلَآ أَنْ هَدَىٰنَا اَللَّهُۖ لَقَدْ جَآءَتْ رُسُلُ رَبِّنَا بِالْحَقِّۖ
وَنُودُوٓاْ أَن تِلْكُمُ اُلْجَنَّةُ أُورِثْتُمُوهَا بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَۖ 42

36. Ubangiji zaice (dasu ranar Alƙiyama) "Ku shiga cikin wuta cikin jumlar al'ummomi waɗanda suka wuce gabanku na aljannu da mutane) Ko yaushe al'umma ta shiga wuta, saita tsine wa "yar uwarta (wacce take gabanta don tayi mata masabbabiyar ɓata). Har Lokacin da suka ruguntsuma cikinta bakiɗaya, al'ummar ƙarshen su, (sune mabiya) saita faɗa ga ta farkonsu (sune waɗanda ake bi) Ya Ubangijinmu waɗannan ne suka ɓatar da mu, basu azaba abar ninkawa ta wuta.

37. Sai Ubangiji yace, "Azaba abar ninkawa ta tabbata ga kowane ɗayanku, sai dai baku san haka ba".

38. Ta farkonsu ta faɗa ga ta karshensu, "Ba wani fifiko da kuke dashi a kanmu (don baku kafirta saboda mu ba, da mu daku ,duk ɗaya ne". (Sai Ubangiji yace dasu,) "To, ku ɗanɗani azaba saboda abinda kuka kasance kuna tsuwurwurta".

(SAKAMAKON KAFIRAI)

39. Haƙiƙa waɗanda suka karyata ayoyinmu sukayi girman kai ga buranta baza a buɗe musu kofofin sama ba, (yayin da aka hau da rayukansu zuwa gareta bayan mutuwa, sai a runtumo su izuwa Sijjina(1), mumini kuwa sai a bude masa kofa a hau da ransa izuwa sama ta bakwai tamfar yadda yazo cikin Hadisi). Bazasu shiga aljanna ba sai raƙumi ya shiga ta kafar allura (kamar yadda Hausawa suke cewa sai jaki ya tsiri kaho, wato bazasu shiga aljannaba har abada) Haka nan muke sakawa ma'abuta Laifi kafirai.

40. Suna dashinfiɗa ta jahannama a birbishinsu akwai mayafai na wuta. Irin wannan sakamako muke sakawa kafirai.

(SAKAMAKON MUMINAI)

41. Waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagari, Barna kallafa wa kowa sai gwargwadon ikonsa. Waɗancananka sune "yan aljanna. sune masu dawwama a cikinta.

42. Mun zare abinda yake cikin ƙirazansu na gilli (wato hako wanda yake tsakaninsu a duniya). ƙoramai suna kwarara ƙarƙashinsu, suka faɗa (yayin da suka tabbata a gidajensu na aljanna,) "Godiya ta tabbata ga Allah wanda ya shirye mu izuwa wannan (aiki, wanda muka sami wannan sakamako saboda shi). Bazamu iya shiriya ba, ba don Allah ya shirye mu ba. Haƙiƙa manzannin Ubangijinmu sun zoda gaskiya, akayi shela cewa wancananka aljanna an gadar mukuda ita ne saboda abinda kuka kasance kuna aikatawa.

(MAHAWARA TSAKANIN "YAN ALJANNA DA "YAN WUTADA "YAN LA'ARAFI)

1) Wato kur kunkun' yan wuta.

وَنَادَىٰ أَصْحَٰبُ الْجَنَّةِ أَصْحَٰبَ النَّارِ أَن قَدْ وَجَدْنَا مَا وَعَدَنَا
رَبُّنَا حَقّاً فَهَلْ وَجَدتُّم مَّا وَعَدَ رَبُّكُمْ حَقّاً قَالُواْ نَعَمْ فَأَذَّنَ مُؤَذِّنُۢ
بَيْنَهُمْ أَن لَّعْنَةُ اللَّهِ عَلَى الظَّٰلِمِينَ ﴿43﴾ الَّذِينَ يَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ
اللَّهِ وَيَبْغُونَهَا عِوَجاً وَهُم بِالْآخِرَةِ كَٰفِرُونَ ﴿44﴾ وَبَيْنَهُمَا حِجَابٌ
وَعَلَى الْأَعْرَافِ رِجَالٌ يَعْرِفُونَ كُلّاً بِسِيمَٰهُمْ
وَنَادَوْاْ أَصْحَٰبَ الْجَنَّةِ أَن سَلَٰمٌ عَلَيْكُمْ لَمْ يَدْخُلُوهَا
وَهُمْ يَطْمَعُونَ ﴿45﴾ * وَإِذَا صُرِفَتْ أَبْصَٰرُهُمْ تِلْقَاءَ أَصْحَٰبِ النَّارِ
قَالُواْ رَبَّنَا لَا تَجْعَلْنَا مَعَ الْقَوْمِ الظَّٰلِمِينَ ﴿46﴾ وَنَادَىٰ أَصْحَٰبُ الْأَعْرَافِ
رِجَالاً يَعْرِفُونَهُم بِسِيمَٰهُمْ قَالُواْ مَا أَغْنَىٰ عَنكُمْ جَمْعُكُمْ وَمَا كُنتُمْ
تَسْتَكْبِرُونَ ﴿47﴾ أَهَٰؤُلَاءِ الَّذِينَ أَقْسَمْتُمْ لَا يَنَالُهُمُ اللَّهُ بِرَحْمَةٍ
ادْخُلُواْ الْجَنَّةَ لَا خَوْفٌ عَلَيْكُمْ وَلَا أَنتُمْ تَحْزَنُونَ ﴿48﴾
وَنَادَىٰ أَصْحَٰبُ النَّارِ أَصْحَٰبَ الْجَنَّةِ أَنْ أَفِيضُواْ عَلَيْنَا مِنَ الْمَاءِ
أَوْ مِمَّا رَزَقَكُمُ اللَّهُ قَالُواْ إِنَّ اللَّهَ حَرَّمَهُمَا عَلَى الْكَٰفِرِينَ ﴿49﴾
الَّذِينَ اتَّخَذُواْ دِينَهُمْ لَهْواً وَلَعِباً وَغَرَّتْهُمُ الْحَيَوٰةُ الدُّنْيَا فَالْيَوْمَ نَنسَىٰهُمْ
كَمَا نَسُواْ لِقَاءَ يَوْمِهِمْ هَٰذَا وَمَا كَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يَجْحَدُونَ ﴿50﴾

ربع

43. "Yan aljanna suka kirawo "yan wuta (wato don muzantawa garesu) mun sami abinda Ubangijinmu yayi mana alƙawari gaskiya. Shin kun sami abinda Ubangijinku ya yi muku alƙawari gaskiya? Sukace "Na'am". Sai mai shela yayi shela tsakaninsu cewa La'anar Allah ta tabbata ga azzalumai!.
44. Waɗanda suke hana mutane bin addinin Allah suke neman hanyar Allah a karkace, su basu bada gaskiya da ranar Lahira ba (kamar yadda Kiristada ire -irensu suke yi mana a yanzu).
45. A tsakaninsu ("yan wutada "yan aljanna) akwai katangar La'arafi, a kan wannan katanga ta aljanna akwai jarumai (da hasanarsu da sayyi'arsu tayi daidai, sunsan kowane daga ɗan aljanna da ɗan wutada ala-marsu, (shine farar fuska ga muminai da baƙar ta ga kafirai, Ance waɗannan jarumai manya - manyan waliyyai masana Allah su ake nufi haka Sufaye suka ce. Allah shi yafi kowa sani). "Yan aljanna sukace gaisuwa ta tabbata gareku, Ubangiji yace, "yan waɗannan katanga basu shiga aljanna ba alhali su suna tsammani a cikin shigarta.
46. Idan an juyar da idanun su "yan La'arafin nan katarnin "ya wuta saisu ce "Ya Ubangijinmu kadaka sanya mu a cikin wuta tareda mutane kafirai".
47. "Yan La'arafin suka kirawo waɗansu mutane na daga "yan wuta, silh san su saboda alamarsu, Sukace, "Tara dukiyar kuda yawan ku bai wadatar daku ,kome ba (daga azabar Allah,) da girman kanku ga buran imani.
48. (Saisu nuno waɗansu raunanan Musulmi su ce musu) "Yanzu waɗannan sune waɗanda kuka rantse cewa Allah bazai samesu da rahamarsa ba. (Ance dasu) Ku shiga aljanna ba tsoro gareku bazakuyi bakin ciki (a Lahira) ba.
49. 'Yan wuta suka kirawo "yan aljanna cewa "Ku kwaro wani abu na ruwa a garemu ko kuma daga abinda Allah ya azurta muku na abinci" Saisu ce, "Haƙiƙa Ubangiji ya haramta su ga kafirai.
50. Waɗanda suka riƙi addininsu shagulgula da wasanni, rayuwar duniya ta ruɗe su (kamar yadda akasarin shiyagabannin duniya na yanzu suke kai na kowane wuri, Inna Lillahi wa inna ilaihi raji'una). A yau zamu barsu a cikin wutamu yi buris dasu,kamar yadda suka bar tanajin saduwa da ranarsu wannan, sukayi buris da tattalin aikin Allah, da musun Ayoyinmu dasuke aikatawa.

(KAFIRAI DA ABINDA SUKE GAMUWA DASHI DA GURCE - GURCENSU)

وَلَقَدْ جِئْنَٰهُم بِكِتَٰبٖ فَصَّلْنَٰهُ عَلَىٰ عِلْمٍ هُدٗى وَرَحْمَةٗ
لِّقَوْمٖ يُؤْمِنُونَ ﴿51﴾ هَلْ يَنظُرُونَ إِلَّا تَأْوِيلَهُۥ يَوْمَ يَأْتِي تَأْوِيلُهُۥ
يَقُولُ الَّذِينَ نَسُوهُ مِن قَبْلُ قَدْ جَآءَتْ رُسُلُ رَبِّنَا بِالْحَقِّ
فَهَل لَّنَا مِن شُفَعَآءَ فَيَشْفَعُواْ لَنَا أَوْ نُرَدُّ فَنَعْمَلَ غَيْرَ الَّذِي
كُنَّا نَعْمَلُ قَدْ خَسِرُواْ أَنفُسَهُمْ وَضَلَّ عَنْهُم مَّا كَانُواْ
يَفْتَرُونَ ﴿52﴾ إِنَّ رَبَّكُمُ اللَّهُ الَّذِي خَلَقَ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضَ
فِي سِتَّةِ أَيَّامٖ ثُمَّ اسْتَوَىٰ عَلَى الْعَرْشِ يُغْشِي اللَّيْلَ النَّهَارَ يَطْلُبُهُۥ
حَثِيثٗا وَالشَّمْسَ وَالْقَمَرَ وَالنُّجُومَ مُسَخَّرَٰتٍ بِأَمْرِهِۦ أَلَا لَهُ الْخَلْقُ
وَالْأَمْرُ تَبَٰرَكَ اللَّهُ رَبُّ الْعَٰلَمِينَ ﴿53﴾ * ادْعُواْ رَبَّكُمْ
تَضَرُّعٗا وَخُفْيَةً إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ الْمُعْتَدِينَ ﴿54﴾ وَلَا تُفْسِدُواْ فِي الْأَرْضِ
بَعْدَ إِصْلَٰحِهَا وَادْعُوهُ خَوْفٗا وَطَمَعًا إِنَّ رَحْمَتَ اللَّهِ
قَرِيبٞ مِّنَ الْمُحْسِنِينَ ﴿55﴾ وَهُوَ الَّذِي يُرْسِلُ الرِّيَٰحَ نُشُرًا
بَيْنَ يَدَيْ رَحْمَتِهِۦ حَتَّىٰ إِذَا أَقَلَّتْ سَحَابٗا ثِقَالٗا سُقْنَٰهُ
لِبَلَدٖ مَّيِّتٖ فَأَنزَلْنَا بِهِ الْمَآءَ فَأَخْرَجْنَا بِهِۦ مِن كُلِّ
الثَّمَرَٰتِ كَذَٰلِكَ نُخْرِجُ الْمَوْتَىٰ لَعَلَّكُمْ تَذَّكَّرُونَ ﴿56﴾

ثمن

51. Hakika mun zo ya mutanen Makka da Littafi da muka rarrabe shi (alkawari da narko da waninsa a bisa sani,) yana mai shiryarwa ga rahama ga mutane muminai.

52. Basa sauraron kome saitawilinsa (wato akibar gargadinsa wato dandanar kudarsa) ranar da gargadinsa zai sauka shine ranar alkiyama. Wadanda sukayi buris dashi tun gabazasu ce, hakika manzannin Ubangijinmu sun zo mana da gaskiya, to, ina zamu sami masu ceto a garemu su cece mu, ko ko za a koma da mu (izuwa duniya) mu yi aiki kyakkyawa ba irin wanda mukayi ba, (sai Ubangiji yace,) "Sun tabar da kawukansu. Abinda suke kirkira (na karya) ya bace musu".

(LA'ILAHA ILLALLAHU 'WATO BA SARKI SAI ALLAH')

53. Hakika Allah ne Ubangijinku (shine) wanda ya halicci sammai da kassai a cikin mikidarm kwana shida (daga kwanukan duniya, wato a cikin gwargwadonta don a Lokacin ba rana, dayaga dama saiya halicce su a cikin kiftawar ido.Yayi haka ne don yakoya mana tafiyasannu -sannu) sannan ya bararraje a kan Al'arshi (bararraza data kamance shi,) yana rufa wa dare rana, kamar yadda yake rufa wa rana dare, kowanne daga dare da rana yana neman dan'uwansa aguje. Da rana da watada taurari ababen horewa ne da umarninsa. To jama'a duk halitta ta Allah ce, duk Lamari na Allah ne, Allah ya kasaita Ubangijin talikai.

(WANI ABU DAGA LADABAN ADDU'A)

54. Ku roki Ubangijinku kuna masu kankan dakai a boye a asirce,Ubangiji ba yason masu shisshigi (a cikin addu'a shine su faifaye a cikin daga murya)

55. Kada kuyi barna a bayan kasa bayan an gyara tada manzanni (da magadansu waliyyai) ku roke shi kuna masu jin tsoro masu kwadayi a cikin rahamarsa, hakika rahamar Allah makusanciyace ga masu kyakkyawan aiki.

(WANI ABU DAGA DALILIN TASHIN ALRIYAMA)

56. Shine wanda yake aiko iskoki ababen daidaitawa nan gaban rahama tasa (wato ruwa,) har yayin data dauki gizagizai masu nauyi da ruwa , sai mu kora girgijen nan izuwa gari matacce wanda babu tsiri a cikinsa, sai mu zubar da ruwa a ciki sai mu fitar saboda ruwan nan daga dukkan nau'i na "ya" yan itatuwa. Tamfar yadda muka fitar da itatuwa nan muke fitar da matattu (daga kaburbura) don ku wa'azantu.

وَالْبَلَدُ الطَّيِّبُ يَخْرُجُ نَبَاتُهُ بِإِذْنِ رَبِّهِ وَالَّذِي خَبُثَ
لَا يَخْرُجُ إِلَّا نَكِدًا كَذَٰلِكَ نُصَرِّفُ الْآيَاتِ لِقَوْمٍ يَشْكُرُونَ ﴿57﴾
لَقَدْ أَرْسَلْنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوْمِهِ فَقَالَ يَا قَوْمِ اعْبُدُوا اللَّهَ
مَا لَكُمْ مِنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُ إِنِّي أَخَافُ عَلَيْكُمْ عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿58﴾
قَالَ الْمَلَأُ مِنْ قَوْمِهِ إِنَّا لَنَرَاكَ فِي ضَلَالٍ مُبِينٍ ﴿59﴾ قَالَ يَا قَوْمِ
لَيْسَ بِي ضَلَالَةٌ وَلَٰكِنِّي رَسُولٌ مِنْ رَبِّ الْعَالَمِينَ ﴿60﴾
أُبَلِّغُكُمْ رِسَالَاتِ رَبِّي وَأَنْصَحُ لَكُمْ وَأَعْلَمُ مِنَ اللَّهِ
مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿61﴾ أَوَعَجِبْتُمْ أَنْ جَاءَكُمْ ذِكْرٌ مِنْ رَبِّكُمْ
عَلَىٰ رَجُلٍ مِنْكُمْ لِيُنْذِرَكُمْ وَلِتَتَّقُوا وَلَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ ﴿62﴾
فَكَذَّبُوهُ فَأَنْجَيْنَاهُ وَالَّذِينَ مَعَهُ فِي الْفُلْكِ وَأَغْرَقْنَا الَّذِينَ
كَذَّبُوا بِآيَاتِنَا إِنَّهُمْ كَانُوا قَوْمًا عَمِينَ ﴿63﴾ * وَإِلَىٰ عَادٍ أَخَاهُمْ
هُودًا قَالَ يَا قَوْمِ اعْبُدُوا اللَّهَ مَا لَكُمْ مِنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُ أَفَلَا تَتَّقُونَ ﴿64﴾
قَالَ الْمَلَأُ الَّذِينَ كَفَرُوا مِنْ قَوْمِهِ إِنَّا لَنَرَاكَ
فِي سَفَاهَةٍ وَإِنَّا لَنَظُنُّكَ مِنَ الْكَاذِبِينَ ﴿65﴾ قَالَ يَا قَوْمِ
لَيْسَ بِي سَفَاهَةٌ وَلَٰكِنِّي رَسُولٌ مِنْ رَبِّ الْعَالَمِينَ ﴿66﴾

ربع

57. Gari daddaɗa mai kyan ƙasa yana fitar da irinsa mai kyau da izinin Ubangijinsa. (mumini ke nan wandazai ji gargaɗi yayi amfani dashi). Wanda ya mugusta kuwa tsirinsa bazai fito ba face a gurɓace, (kafiri ke nan da gargaɗi bazai amfane shi ba). Tamfar da muka bayyana abin nan da muka ambata muke bayyana ayoyi ga mutane masu tsoron Allah.

(ƘISSAR ANNABI NUHU ALAIHISSALAM) WADDATA ƘUNSHI KUJI TSORON ALLAH DON KU SAMI JINƘANSA

58. Haƙiƙa mun aiko Annabi Nuhu (Alaihissalam izuwa mutanensa, yace "Yaku mutanena ku bautawa Allah, bakuda wani Ubangiji bashi ba, haƙiƙa ni ina jin tsoron rana maigirma a gareku, (in kun bautawa waninsa)".
59. Manya - manya daga mutanensa Sukace, "Haƙiƙa mu muna ganinka a cikin ɓata mabayyani".
60. yace "Yaku mutanena ba ɓata gareni, sai dai ni manzo ne daga Ubangijin talikai.
61. "Ina iyar muku sakonnin Ubangijina, inayi muku nasiha. ina sanin abinda baku sani badaga Ubangiji.
62. "Donme zaku ƙaryata, kukayi mana ki don gargaɗi yazo muku daga Ubangijinku a bisa harshen mutum daga cikinku, donya tsoratar daku ,azabar Allah? Kuji tsoron Allah don ku sami rahamarsa".
63. Sai suka ƙaryata shi, sai muka tserar dashi daga nutsewa tareda waɗanda suke tare dashi a cikin jirgi, muka nutsar da waɗanda suka ƙaryatada ayoyinmu (da ruwan Dufanu). Haƙiƙia su sun kasance mutane makafi (ga buran gaskiya).

(ƘISSAR ANNABI HUDU ALAIHISSALAM) WADDATA ƘUNSHI KOMAI ƘARFIN DAULA IDAN TAYI KARO DA ALLAH TA RUSHE

64. Mun aiko Annabi Hudu (Alaihissalam) izuwa Adu (ta farko) ɗan uwansu (a ƙabila,) yace, "Yaku mutanena ku bautawa Allah, bakuda wani Ubangiji bashi ba. Donme ba kwa tsoronsa?".
65. Manya - manya daga waɗanda suka kafirta Sukace, "Haƙiƙa mu muna ganin ka a cikin wauta. Haƙiƙa mu muna zaton ka daga marasa gaskiya (a cikin aike)".
66. Yace, "Yaku mutanena, ba wauta gareni sai dai ni jakada ne daga Ubangijin talikai.

أُبَلِّغُكُمْ رِسَٰلَٰتِ رَبِّيَ وَأَنَا لَكُمْ نَاصِحٌ أَمِينٌ ﴿67﴾ أَوَعَجِبْتُمُۥٓ
أَن جَآءَكُمْ ذِكْرٌ مِّن رَّبِّكُمْ عَلَىٰ رَجُلٍ مِّنكُمْ لِيُنذِرَكُمْ
وَاذْكُرُوٓاْ إِذْ جَعَلَكُمْ خُلَفَآءَ مِنۢ بَعْدِ قَوْمِ نُوحٍ
وَزَادَكُمْ فِي الْخَلْقِ بَصْطَةً فَاذْكُرُوٓاْ ءَالَآءَ اللَّهِ
لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿68﴾ قَالُوٓاْ أَجِئْتَنَا لِنَعْبُدَ اللَّهَ وَحْدَهُۥ
وَنَذَرَ مَا كَانَ يَعْبُدُ ءَابَآؤُنَا فَأْتِنَا بِمَا تَعِدُنَآ
إِن كُنتَ مِنَ الصَّٰدِقِينَ ﴿69﴾ قَالَ قَدْ وَقَعَ عَلَيْكُم مِّن رَّبِّكُمْ
رِجْسٌ وَغَضَبٌ أَتُجَٰدِلُونَنِي فِي أَسْمَآءٍ سَمَّيْتُمُوهَآ أَنتُمْ
وَءَابَآؤُكُم مَّا نَزَّلَ اللَّهُ بِهَا مِن سُلْطَٰنٍ فَانتَظِرُوٓاْ إِنِّي
مَعَكُم مِّنَ الْمُنتَظِرِينَ ﴿70﴾ فَأَنجَيْنَٰهُ وَالَّذِينَ مَعَهُۥ بِرَحْمَةٍ مِّنَّا
وَقَطَعْنَا دَابِرَ الَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَمَا كَانُواْ
مُؤْمِنِينَ ﴿71﴾ وَإِلَىٰ ثَمُودَ أَخَاهُمْ صَٰلِحًا قَالَ يَٰقَوْمِ اعْبُدُواْ اللَّهَ
مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥ قَدْ جَآءَتْكُم بَيِّنَةٌ مِّن رَّبِّكُمْ
هَٰذِهِۦ نَاقَةُ اللَّهِ لَكُمْ ءَايَةً فَذَرُوهَا تَأْكُلْ فِي أَرْضِ اللَّهِ
وَلَا تَمَسُّوهَا بِسُوٓءٍ فَيَأْخُذَكُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿72﴾

67. "Ina iyar muku sakonnin Ubangijina. Ni mai nasiha ne a gareku, amintacce (a kan aike).
68. "Donme kukayi mana ki don gargaɗi yazo muku daga Ubangijinku a bisa harshen mutum daga gareku, donya tsoratar daku ,Allah. Ku tuna zamanin dayasanya ku mana ya a cikin ƙasa bayan mutanen Annabi Nuhu, ya ƙara muku ƙarfi a cikin halittada tsawo, (dogonsu zira'i ɗari, gajerensu kamu sittin). Ku tuna ni'imomin Allah a gareku don ku sami rabauta.
69. Sukace "Kazo mana ne don mu bautawa Allah shi kaɗai, mubar abinda iyayenmu suke bautawa? To, zo mana da abinda kakeyi mana alwashi dashi (na azaba,) in ka kasance cikin magaskata".
70. Yace, "Azabata auku a gareku daga Ubangijinkuda fushinsa. Yaya zaku dinga jayayya dani a cikin sunannakin da kuka ƙage su kuda iyayen ku, (wato gumaka da kuke bauta musu,) da Allah bai saukar da wata hujja a kan a bauta musu ba. To, ku saurari azaba, haƙiƙa ni taredaku ,ina cikin masu sauraro."
71. Aka aiko musu iska bakarara, muka tserar da Annabi Hudu da waɗanda suke tare dashi (na daga muminai.) da rahama daga garemu. Muka tunɓuke asalin waɗannan da suka ƙaryata ayoyinmu, basu kasance muminai ba.

(ƘISSAR ANNABI SALIHU ALAIHISSALAM TAREDA MUTANENSA) WADDATA ƘUNSHI KOMAI KARFIN DAULA IDAN TA RAINA MAI NASIHA DON ALLAH, ALLAH YA TUNBUKE TA.

72. Haƙiƙa mun aiko Annabi Salihu (Alaihissalam) izuwa Samudawa ɗan uwansu (a ƙabila,) yace, "Yaku mutanena ku bautawa Allah, bakuda wani Ubangiji bashi ba. Mu'ujiza tazo muku daga Ubangijinku (a bisa gaskiyata). Wannan tagu-war Allah ce, aya a gareku. (Sun roƙe shi yafito musu da ita daga wata Fa da suka nuna). Ku bar ta tayi kiwo a cikin ƙasar Allah kadaku ,shafe tada mummuna (duka ko sarewa) bare azaba mai raɗaɗi ta kama ku.

ثمن

وَاذْكُرُوا إِذْ جَعَلَكُمْ خُلَفَآءَ مِنۢ بَعْدِ عَادٍ
وَبَوَّأَكُمْ فِي الْأَرْضِ تَتَّخِذُونَ مِن سُهُولِهَا
قُصُورًا وَتَنْحِتُونَ الْجِبَالَ بِيُوتًا فَاذْكُرُوا ءَالَآءَ
اللَّهِ وَلَا تَعْثَوْا فِي الْأَرْضِ مُفْسِدِينَ (73) * قَالَ الْمَلَأُ الَّذِينَ
اسْتَكْبَرُوا مِن قَوْمِهِ لِلَّذِينَ اسْتُضْعِفُوا لِمَنْ ءَامَنَ
مِنْهُمْ أَتَعْلَمُونَ أَنَّ صَالِحًا مُّرْسَلٌ مِّن رَّبِّهِ قَالُوا إِنَّا بِمَا
أُرْسِلَ بِهِ مُؤْمِنُونَ (74) قَالَ الَّذِينَ اسْتَكْبَرُوا إِنَّا بِالَّذِي
ءَامَنتُم بِهِ كَافِرُونَ (75) فَعَقَرُوا النَّاقَةَ وَعَتَوْا عَنْ أَمْرِ
رَبِّهِمْ وَقَالُوا يَا صَالِحُ ائْتِنَا بِمَا تَعِدُنَا إِن كُنتَ مِنَ
الْمُرْسَلِينَ (76) فَأَخَذَتْهُمُ الرَّجْفَةُ فَأَصْبَحُوا فِي دَارِهِمْ
جَاثِمِينَ (77) فَتَوَلَّى عَنْهُمْ وَقَالَ يَا قَوْمِ لَقَدْ أَبْلَغْتُكُمْ رِسَالَةَ
رَبِّي وَنَصَحْتُ لَكُمْ وَلَكِن لَّا تُحِبُّونَ النَّاصِحِينَ (78) وَلُوطًا
إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِ أَتَأْتُونَ الْفَاحِشَةَ مَا سَبَقَكُم بِهَا
مِنْ أَحَدٍ مِّنَ الْعَالَمِينَ (79) إِنَّكُمْ لَتَأْتُونَ الرِّجَالَ
شَهْوَةً مِّن دُونِ النِّسَآءِ بَلْ أَنتُمْ قَوْمٌ مُّسْرِفُونَ (80)

73. "Ku tuna zamanin dayasanya ku mana ya a bayan ƙasa bayan Adawa, Ya zaunar daku ,a cikin ƙasa kuna riƙon gidaje daga tattausar ƙasarta (a zamanin zafi) kuna sassaƙa gidaddajin duwarwatsu (a zamanin ɗari). Ku tuna ni'imomin Allah kada kuyi ɓarna a bayan kasa, kar kuyi ɓarna!"

74. Manyan mutane waɗanda suka girman kai daga mutanensa suka faɗa ga waɗannan dasuke raunana na waɗanda suka bada gaskiya daga cikinsu ai kun sani shi Annabi Salihu jakada ne daga Ubangijinsa, izuwa gareku. Sukace "I, mu haƙiƙa mun bada gaskiya da abinda aka aiko shi dashi".

75. Sai waɗanda sukayi girman kai Sukace, "Mu bamu bada gaskiya da abinda kuka bada gaskiya dashi ba".

76. (Da can taguwar tana da rana ta shan ruwa su kuma suna da ranar shan ruwa, suka ƙosa) suka kashe taguwar (ranar Laraba, ƙudaru ne ya kashe tada Umarninsu) sukayi tawaye daga al'amarin Ubangijinsu Sukace, "Ya Salihu zo mana da abinda kake bamu tsoro dashi (na azaba,) in ka kasance daga ma'aika.

77. Sai girgiza mai ƙarfi daga ƙasa da tsawa daga sama mai tsanani ta same su, suka zama halakakku suna durƙushe a kan gwiwoyinsu a cikin gidajensu.

78. Annabi Salihu ya rabu dasu, yace, "Yaku mutanena haƙiƙa na iyar mukuda aiken Ubangijina, nayi muku nasiha, amma ba kwa son masu nasiha".

(ƘISSAR ANNABI LUƊU ALAIHISSALAM) WANDA YAKUNSHI DU WANDA YAGA BAKON SABO A GABA, YAGAMU DA BAKON SAKAMAKO MUMMUNA

79. Ka ambaci Annabi Luɗu (Alaihissalam) zamanin dayace da mutanensa, "Donme kuke aikata alfasha, (zuwa wa mazaje ta bayansu) ɗaya daga cikin talikai bai taɓa rigayar kuda ita ba, (mutum ko aljan).

80. "Donme kuke zuwa wa maza don sha'awa ba mata ba? Kai! ku dai mutane ne maɓarnata".

وَمَا كَانَ جَوَابَ قَوْمِهِۦٓ إِلَّآ أَن قَالُوٓاْ أَخْرِجُوهُم
مِّن قَرْيَتِكُمْ إِنَّهُمُۥٓ أُنَاسٞ يَتَطَهَّرُونَ ﴿81﴾ فَأَنجَيْنَٰهُ
وَأَهْلَهُۥٓ إِلَّا امْرَأَتَهُۥ كَانَتْ مِنَ الْغَٰبِرِينَ ﴿82﴾ وَأَمْطَرْنَا
عَلَيْهِم مَّطَراٗ فَانظُرْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ
الْمُجْرِمِينَ ﴿83﴾ وَإِلَىٰ مَدْيَنَ أَخَاهُمْ شُعَيْباٗ قَالَ
يَٰقَوْمِ اعْبُدُواْ اللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥ قَدْ جَآءَتْكُم
بَيِّنَةٞ مِّن رَّبِّكُمْ فَأَوْفُواْ الْكَيْلَ وَالْمِيزَانَ
وَلَا تَبْخَسُواْ النَّاسَ أَشْيَآءَهُمْ وَلَا تُفْسِدُواْ فِي الْأَرْضِ
بَعْدَ إِصْلَٰحِهَا ذَٰلِكُمْ خَيْرٞ لَّكُمْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿84﴾
وَلَا تَقْعُدُواْ بِكُلِّ صِرَٰطٖ تُوعِدُونَ وَتَصُدُّونَ
عَن سَبِيلِ اللَّهِ مَنْ ءَامَنَ بِهِۦ وَتَبْغُونَهَا عِوَجاٗ
وَاذْكُرُواْ إِذْ كُنتُمْ قَلِيلاٗ فَكَثَّرَكُمْ وَانظُرُواْ كَيْفَ كَانَ
عَٰقِبَةُ الْمُفْسِدِينَ ﴿85﴾ وَإِن كَانَ طَآئِفَةٞ مِّنكُمْ ءَامَنُواْ
بِالَّذِيٓ أُرْسِلْتُ بِهِۦ وَطَآئِفَةٞ لَّمْ يُؤْمِنُواْ فَاصْبِرُواْ
حَتَّىٰ يَحْكُمَ اللَّهُ بَيْنَنَا وَهُوَ خَيْرُ الْحَٰكِمِينَ ﴿86﴾

81. Ba wani abu daya zama jawabin mutanensa, sai fadinsu ku fitar dasu Annabi Ludu da mabiyansa daga alƙaryarku. Haƙiƙa su mutane ne dasuke tsarkaka (ga buran bayan maza)".

82. Sai Muka tserar dashi da iyalinsa, sai matarsa. Ta kasance cikin masu wanzuwa cikin azaba.

83. Kuma muka tsuge da ruwa a kansu (na ƙonannen dutse, muka halakar dasu). ka duba, ƙaƙa ƙarshen masu Laifi ya kasance?

(ƘISSAR ANNABI SHU'AIBU ALAIHISSALAM) WANDA BAI JIƘAN BAY IN, ALLAH BA, ALLAH BAZAI JIƘAN SABA

84. Mun aiko Annabi Shu'aibu izuwa Madayana ɗan uwansu, yace, "Yaku mutanena ku bau-tawa Allah, bakuda wani Ubangiji sai shi. Mu'ujiza tazo muku daga Ubangijinku (a kan gaskiyata). Ku cika mudu da ma'auni kadaku ,tauye wa mutane kayayyakinsu, kada kuyi ɓarna a bayan ƙasa da kafirci da saɓo bayan an gyara tada Annabawa. Wancananku shi yafi amfani gareku in kun kasance muminai. To, ku aikata abinda muka umarce ku".

(HARAMCIN KWACE DA KWASTAN)

85. Kadaku, zauna a kowace hanYakuna ba mutane tsoro (da karɓe dukiyoyinsu ko yi musu kwastan,) kuna tsare wanda ya bada gaskiyaga buran addinin Allah. (Kunayi masa narko da kisa) kuna kwatantata tafarkin Allah a karkace. Ku tuna zamanin da kuka kasance kaɗan, ya yawaita ku. Ku duba ƙaƙa ƙarshen maɓarnata ya kasance?

86. Idan waɗansu mutane daga gareku sun bada gaskiya da abinda aka aiko ni dashi, waɗansu kuma basu bada gaskiya dashi ba! To, ku daure har Allah yayi hukunci tsakaninmu daku ,(da halakar da mai ƙarya da tserar da mai gaskiya). Allah shine mafi mahukunta iya hukunci (wato shine mafi adalci).

حزب

۞ قَالَ ٱلْمَلَأُ ٱلَّذِينَ ٱسْتَكْبَرُواْ مِن قَوْمِهِۦ لَنُخْرِجَنَّكَ يَٰشُعَيْبُ وَٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ مَعَكَ مِن قَرْيَتِنَا أَوْ لَتَعُودُنَّ فِي مِلَّتِنَا قَالَ أَوَلَوْ كُنَّا
كَٰرِهِينَ ﴿87﴾ قَدِ ٱفْتَرَيْنَا عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا إِنْ عُدْنَا فِي مِلَّتِكُم
بَعْدَ إِذْ نَجَّىٰنَا ٱللَّهُ مِنْهَا وَمَا يَكُونُ لَنَا أَن نَّعُودَ فِيهَا إِلَّا
أَن يَشَاءَ ٱللَّهُ رَبُّنَا وَسِعَ رَبُّنَا كُلَّ شَيْءٍ عِلْمًا عَلَى ٱللَّهِ تَوَكَّلْنَا
رَبَّنَا ٱفْتَحْ بَيْنَنَا وَبَيْنَ قَوْمِنَا بِٱلْحَقِّ وَأَنتَ خَيْرُ ٱلْفَٰتِحِينَ ﴿88﴾
وَقَالَ ٱلْمَلَأُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن قَوْمِهِۦ لَئِنِ ٱتَّبَعْتُمْ شُعَيْبًا
إِنَّكُمْ إِذًا لَّخَٰسِرُونَ ﴿89﴾ فَأَخَذَتْهُمُ ٱلرَّجْفَةُ فَأَصْبَحُواْ
فِي دَارِهِمْ جَٰثِمِينَ ﴿90﴾ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ شُعَيْبًا كَأَن لَّمْ يَغْنَوْاْ فِيهَا
ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ شُعَيْبًا كَانُواْ هُمُ ٱلْخَٰسِرِينَ ﴿91﴾ فَتَوَلَّىٰ عَنْهُمْ
وَقَالَ يَٰقَوْمِ لَقَدْ أَبْلَغْتُكُمْ رِسَٰلَٰتِ رَبِّي وَنَصَحْتُ لَكُمْ فَكَيْفَ
ءَاسَىٰ عَلَىٰ قَوْمٍ كَٰفِرِينَ ﴿92﴾ وَمَا أَرْسَلْنَا فِي قَرْيَةٍ مِّن نَّبِيءٍ
إِلَّا أَخَذْنَا أَهْلَهَا بِٱلْبَأْسَاءِ وَٱلضَّرَّاءِ لَعَلَّهُمْ يَضَّرَّعُونَ ﴿93﴾ ثُمَّ
بَدَّلْنَا مَكَانَ ٱلسَّيِّئَةِ ٱلْحَسَنَةَ حَتَّىٰ عَفَواْ وَّقَالُواْ قَدْ مَسَّ ءَابَاءَنَا
ٱلضَّرَّاءُ وَٱلسَّرَّاءُ فَأَخَذْنَٰهُم بَغْتَةً وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿94﴾

87. Manyan mutane waɗanda sukayi girman kai gaburan imani daga mutanensa Sukace, "Lallai zamu fitar dakai ya Shu'aibu da waɗanda suka bada gaskiya dakai daga alƙaryarmu, koku zamo cikin addininmu". Yace, "Yanzu ma zamo a cikin addininku koda mun kasance Barna bukata.
88. "Haƙiƙa mun ƙirƙiri ƙarya bisa Allah in mun zamo cikin addininku, bayan Allah ya tserar da mu daga gareta. Bazai yiwu garemu mu zamo cikin ta ba sai in Allah Ubangijinmu yaga dama. Ilimin Ubangijinmu ya yalwaci komai, (ga Allah kaɗai muka dogara. ya Ubangijinmu yi hukunci tsakaninmu da mutanenmu da gaskiya. kaine mafificin mahukunta".

(ƘARSHEN KAFIRAI NA MUTANEN ANNABI SHU'AIBU)

89. Manyan mutane daga waɗanda suka kafirta daga mutanensa Sukace, "Wallahi in kun bi Shu'aibu yayin nan Lalle ku taɓaɓɓu ne".
90. Sai girgiza mai tsanani ta sauka a garesu, suka zama halakakku a durkushe a cikin gidajensu.
91. Waɗanda suka ƙaryata Annabi Shu'aibu kamar basu taɓa zama a gidaddajinsu ba. Waɗanda suka ƙaryata Annabi Shu'aibu, haƙiƙa su sun kasance taɓaɓɓu.
92. Saiya rabu dasu, yace "Yaku mutanena haƙiƙa na iyar mukuda aiken Ubangijina, nayi muku nasiha, baku bada gaskiya ba. To, yaya zan yi baƙin ciki a kan mutane kafirai?".

(AL'ADAR ALLAH A CIKIN HALITTA)

93. Bamu aiko wani Annabi a cikin alƙarya basu ka ƙaryata shi, face mun halakar da mutanentada tsananin talauci, da rashin lafiya donsu rusuna wa Allah su bada gaskiya.
94. Sannan muka basu lafiya da wadata maimakon azabar nan, har suka farfado suka yawaita, suka faɗa don butulci ga ni'ima,rashin lafiya da ma ya saml iyayenmu da tsananin talauci tamfar daya same mu, wannan al'adar -duniyace ba uƙuba ce ba, kai mu koma kan bakanmu. Sai Ubangiji yace, "Sai muka ƙar musu da azaba baraɓe, take, alhali basu san zamanin data sauka garesu ba.

(AL'ADAR ALLAH A CIKIN HALITTA HAR YAU)

وَلَوْ أَنَّ أَهْلَ الْقُرَىٰ ءَامَنُوا وَاتَّقَوْا لَفَتَحْنَا عَلَيْهِم بَرَكَٰتٍ
مِّنَ السَّمَاءِ وَالْأَرْضِ وَلَٰكِن كَذَّبُوا فَأَخَذْنَٰهُم بِمَا
كَانُوا يَكْسِبُونَ (95) أَفَأَمِنَ أَهْلُ الْقُرَىٰ أَن يَأْتِيَهُم بَأْسُنَا
بَيَٰتًا وَهُمْ نَآئِمُونَ (96) أَوَأَمِنَ أَهْلُ الْقُرَىٰ أَن يَأْتِيَهُم بَأْسُنَا
ضُحًى وَهُمْ يَلْعَبُونَ (97) أَفَأَمِنُوا مَكْرَ اللَّهِ فَلَا يَأْمَنُ مَكْرَ اللَّهِ
إِلَّا الْقَوْمُ الْخَٰسِرُونَ (98) * أَوَلَمْ يَهْدِ لِلَّذِينَ يَرِثُونَ الْأَرْضَ ثمن
مِنۢ بَعْدِ أَهْلِهَا أَن لَّوْ نَشَآءُ أَصَبْنَٰهُم بِذُنُوبِهِمْ وَنَطْبَعُ عَلَىٰ
قُلُوبِهِمْ فَهُمْ لَا يَسْمَعُونَ (99) تِلْكَ الْقُرَىٰ نَقُصُّ عَلَيْكَ
مِنْ أَنۢبَآئِهَا وَلَقَدْ جَآءَتْهُمْ رُسُلُهُم بِالْبَيِّنَٰتِ فَمَا
كَانُوا لِيُؤْمِنُوا بِمَا كَذَّبُوا مِن قَبْلُ كَذَٰلِكَ يَطْبَعُ
اللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِ الْكَٰفِرِينَ (100) وَمَا وَجَدْنَا لِأَكْثَرِهِم
مِّنْ عَهْدٍ وَإِن وَجَدْنَا أَكْثَرَهُمْ لَفَٰسِقِينَ (101) ثُمَّ بَعَثْنَا
مِنۢ بَعْدِهِم مُّوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَا إِلَىٰ فِرْعَوْنَ وَمَلَإِيْهِۦ فَظَلَمُوا
بِهَا فَانظُرْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ الْمُفْسِدِينَ (102) وَقَالَ
مُوسَىٰ يَٰفِرْعَوْنُ إِنِّيَ رَسُولٌ مِّن رَّبِّ الْعَٰلَمِينَ (103)

95. Da dai cewa mazowa alƙaryatu masu ƙaryatawa sun bada gaskiya da Allah da manzanninsa sun ji tsoron Allah; da mun buɗe musu albarkatan sama, mu saukar da ruwa da albarkatan ƙasa, mu saukar da ruwa da albarkatan ƙasa, (yafitar da tsiri). To, sai dai sun ƙaryata (manzanni,) sai muka far musu da azaba saboda abinda suka kasance suna aikatawa.

96. Yanzu mutanen mazowa alƙaryatu sun amince azabarmu tazo musu da dare, alhali suna barci?

97. Ko ma'abuta alƙaryatu sun amince azabarmu tazo musu da rana, alhali suna wasanni?

98. Ko sun amince maƙarƙashiyar Allah ne? To, ba mai amince maƙarƙashiyar Allah sai mutane taɓaɓɓu.

99. Shin bai bayyana bane ga waɗanda suke gadon ƙasa bayan halakar mutanentacewa da mun ga dama da mun far musu da azaba, saboda zunubansu, (tamfar yadda muka far wa waɗanda suke gabansu). Mune muke yumƙewa bisa zukatansu, to, su basa jin gargaɗi. (Allah ya kiyashe mu Amin).

(IZNA A CIKIN ƘISSOSHIN WAƊANDA SUKA WUCE)

100. Waɗancananka alƙaryatu muna Labarta maka (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama) daga Labaran mutanenta, haƙiƙa manzjanninsu sun zo musu da mu'ujizozi mabayyana, basu kasance suna bada gaskiyaga abinda suka ƙaryata dashi ba tun gaban zuwansu ba sai suka zarce a kan kafircinsu. Kamar wancananka yimkiya Allah yake yimkewa a bisa zukatan kafirai.

101. Bamu sami cika alƙawari na ranar ALASTU BI RABBIKUM daga yawaicin mutane ba. Haƙiƙa mun sami yawaicinsu fasiƙai ne.

(ƘISSAR ANNABI MUSA ALAIHISSALAM WACCE TA KUNSHI YAWAN AYO YI BASHINE SHIRIYA BASHIRIYA DAGA ALLAH TAKE, ALLAH YA SHIRYE MU AMIN. KYAK KY AWAN KARSHE YA TAB-BATA GA MASU TSORAN ALLAH)

102. Sannan muka aiko Annabi Musa (Alaihissalam) bayan waɗannan manzanni da ayoyinmu (guda tara izuwa Fir'auna da muianensa suka kafirce da ita. Duba ƙaƙa ƙarshen maɓarnata ya kasance

103. Annabi Musa (Alaihissalam) yace; "Yafir'auna, nijakada ne daga Ubangijin talikai (izuwa gareka," saiya ƙaryata shi).

حَقِيقٌ عَلَىٰ أَن لَّا أَقُولَ عَلَى اللَّهِ إِلَّا الْحَقَّ قَدْ جِئْتُكُم
بِبَيِّنَةٍ مِّن رَّبِّكُمْ فَأَرْسِلْ مَعِيَ بَنِي إِسْرَائِيلَ ﴿104﴾ قَالَ إِن كُنتَ
جِئْتَ بِآيَةٍ فَأْتِ بِهَا إِن كُنتَ مِنَ الصَّادِقِينَ ﴿105﴾ فَأَلْقَىٰ
عَصَاهُ فَإِذَا هِيَ ثُعْبَانٌ مُّبِينٌ ﴿106﴾ وَنَزَعَ يَدَهُ فَإِذَا هِيَ
بَيْضَاءُ لِلنَّاظِرِينَ ﴿107﴾ قَالَ الْمَلَأُ مِن قَوْمِ فِرْعَوْنَ إِنَّ هَٰذَا
لَسَاحِرٌ عَلِيمٌ ﴿108﴾ يُرِيدُ أَن يُخْرِجَكُم مِّنْ أَرْضِكُمْ فَمَاذَا
تَأْمُرُونَ ﴿109﴾ قَالُوا أَرْجِهْ وَأَخَاهُ وَأَرْسِلْ فِي الْمَدَائِنِ حَاشِرِينَ ﴿110﴾
يَأْتُوكَ بِكُلِّ سَاحِرٍ عَلِيمٍ ﴿111﴾ وَجَاءَ السَّحَرَةُ فِرْعَوْنَ
قَالُوا إِنَّ لَنَا لَأَجْرًا إِن كُنَّا نَحْنُ الْغَالِبِينَ ﴿112﴾ قَالَ نَعَمْ وَإِنَّكُمْ
لَمِنَ الْمُقَرَّبِينَ ﴿113﴾ قَالُوا يَا مُوسَىٰ إِمَّا أَن تُلْقِيَ وَإِمَّا
أَن نَّكُونَ نَحْنُ الْمُلْقِينَ ﴿114﴾ قَالَ أَلْقُوا فَلَمَّا أَلْقَوْا سَحَرُوا
أَعْيُنَ النَّاسِ وَاسْتَرْهَبُوهُمْ وَجَاءُوا بِسِحْرٍ عَظِيمٍ ﴿115﴾
* وَأَوْحَيْنَا إِلَىٰ مُوسَىٰ أَنْ أَلْقِ عَصَاكَ فَإِذَا هِيَ تَلْقَفُ ربع
مَا يَأْفِكُونَ ﴿116﴾ فَوَقَعَ الْحَقُّ وَبَطَلَ مَا كَانُوا يَعْمَلُونَ ﴿117﴾
فَغُلِبُوا هُنَالِكَ وَانقَلَبُوا صَاغِرِينَ ﴿118﴾ وَأُلْقِيَ السَّحَرَةُ سَاجِدِينَ ﴿119﴾

104. (Sai Annabi Musa yace); "Ni dole ne a gareni bazan faɗi komai ga Allah ba sai gaskiya. Haƙiƙa nazo mukuda aya daga Ubangijinku. Ka saki Bani -Isra'ila taredani (izuwa Sham," alhali yana bautar dasu).
105. To, sai Fir'auna yace (dashi,) "In ka kasance ka zoda wata aya (bisa da'awarka,) to, kawo mana ita, in ka kasance daga magaskata (a cikinta)".
106. To, sai Annabi Musa ya jefa sandarsa, sai ga ta macijiya babba.
107. Yafitar da hannunsa (na dama,) da ga aijihunsa sai ga ta fara fat ga masu duba. (Da can kuwa ana ganintajazur).
108. Sai manyan mutane daga mutanen Fir'auna Sukace, "Haƙiƙa wannan Lallai matsafi ne mai zurfi a cikin sanin tsafi.
109. "Yana nufin yafitar daku ,daga ƙasar ku. To, Menene zakuyi umarni (dashi?)"
110. Sai Sukace, "Jinkirta shi da dan'uwansa ka aika a cikin garuruwa kuna masu tara runduna .
111. "Su zo maka da dukkan matsafi mai zurfin sanin tsafi".
112. Matsafa suka zowa Fir'auna, Sukace, "Yanzu muna da Lada in mun kasance marinjaya?"
113. Fir'auna yace "Na'am, haƙiƙa ku kuna daga ababen kusantawa."
114. Sukace, "ya Musa imma ka jefa (sandarka,) ko kuwa mu kasance mune zamu jefa (abinda yake tareda mu)".
115. Yace, "Kujefa".Yayin da suka jefa igiyoyinsu da sandunansu sai suka suddaburance mutane, suka firgita su. ("Yan waɗannan igiyoyi suka kasance suna yawo kamar macizai wul'wul!) suka zoda tsafi maigirma.

(IMANIN MATSAFA GA ANNABI MUSA ALAIHISSALAM DA BAYYANAR GASKIYA)

116. Muka aiko izuwa Annabi Musa cewa jefa sandarka, kumfa sai ga ta tana lanƙwame abinda suke ƙarya (dashi).
117. Sai gaskiya ta tabbata, abinda suke aikatawa na tsafi ya lalace.
118. Aka rinjayi Fir'auna da muta-nensa a cananka suka zamo wulakantattu.
119. Matsafa suka faɗi suna masu sajada.

قَالُوٓاْ ءَامَنَّا بِرَبِّ اِ۬لْعَٰلَمِينَ ﴿120﴾ رَبِّ مُوس۪يٰ وَهَٰرُونَ ﴿121﴾ قَالَ
فِرْعَوْنُ ءَآمَنتُم بِهِۦ قَبْلَ أَنْ ءَاذَنَ لَكُمْ إِنَّ هَٰذَا لَمَكْرٞ مَّكَرْتُمُوهُ
فِے اِ۬لْمَدِينَةِ لِتُخْرِجُواْ مِنْهَآ أَهْلَهَا فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ ﴿122﴾ لَأُقَطِّعَنَّ
أَيْدِيَكُمْ وَأَرْجُلَكُم مِّنْ خِلَٰفٖ ثُمَّ لَأُصَلِّبَنَّكُمْ أَجْمَعِينَ ﴿123﴾
قَالُوٓاْ إِنَّآ إِلَيٰ رَبِّنَا مُنقَلِبُونَ ﴿124﴾ وَمَا تَنقِمُ مِنَّآ إِلَّآ أَنْ ءَامَنَّا
بِـَٔايَٰتِ رَبِّنَا لَمَّا جَآءَتْنَا رَبَّنَآ أَفْرِغْ عَلَيْنَا صَبْراٗ وَتَوَفَّنَا مُسْلِمِينَ ﴿125﴾
وَقَالَ اَ۬لْمَلَأُ مِن قَوْمِ فِرْعَوْنَ أَتَذَرُ مُوس۪يٰ وَقَوْمَهُۥ
لِيُفْسِدُواْ فِے اِ۬لْأَرْضِ وَيَذَرَكَ وَءَالِهَتَكَ قَالَ سَنَقْتُلُ
أَبْنَآءَهُمْ وَنَسْتَحْيِۦ نِسَآءَهُمْ وَإِنَّا فَوْقَهُمْ قَٰهِرُونَ ﴿126﴾
قَالَ مُوس۪يٰ لِقَوْمِهِ اِسْتَعِينُواْ بِاللَّهِ وَاصْبِرُوٓاْ إِنَّ اَ۬لْأَرْضَ
لِلَّهِ يُورِثُهَا مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ وَالْعَٰقِبَةُ لِلْمُتَّقِينَ ﴿127﴾
قَالُوٓاْ أُوذِينَا مِن قَبْلِ أَن تَأْتِيَنَا وَمِنۢ بَعْدِ مَا جِئْتَنَا قَالَ عَس۪يٰ
رَبُّكُمُۥٓ أَنْ يُهْلِكَ عَدُوَّكُمْ وَيَسْتَخْلِفَكُمْ فِے اِ۬لْأَرْضِ
فَيَنظُرَ كَيْفَ تَعْمَلُونَ ﴿128﴾ وَلَقَدْ أَخَذْنَآ ءَالَ فِرْعَوْنَ
بِالسِّنِينَ وَنَقْصٖ مِّنَ اَ۬لثَّمَرَٰتِ لَعَلَّهُمْ يَذَّكَّرُونَ ﴿129﴾

120. Sukace, "Mun bada gaskiya da Ubangijin talikai.
121. "Ubangijin Annabi Musa da Haruna (Alaihimassalam)" saboda sun tabbata abinda suka gani na daga sandasunsan ƙaryaba tayi wannan ba).

(TUHUMAR FIR'AUNA GA MATSAFA)

122. Fir'aunu yace, "Yaya zaku bada gaskiya da Annabi Musa tun gaban bamu yi muki izini ba? Haƙiƙa wannan makirci ne da kuka aikata shi a cikin wannan gari don ku fitar da mutanenta daga cikinta. To, da sannu kwa san (abindazai same ku daga gareni).
123. "Zan yanyanka hannayenkuda kafafuwanku a jirge, (wato hannun kowane ɗaya na dama da kafarsa ta hagu) sannan zan tsire ku bakiɗaya".
124. Sukace, "Mu masu komawa ne zuwa Ubangijinmu, bayan mutuwarmu ta kowane hali.
125. "Baka ƙin?komai daga garemu sai don mun bada gaskiya da ayoyin Ubangijinmu yayin datazo mana. Ya Ubangijinmu kwarara haƙuri a garemu ka ƙarbe mu muna Musulmai".

(ABINDA YA AUKU DAGA AL'AMARIN FIR'AUNA DA MUTANENSA TAREDA ANNABI MUSA ALAIHISSALAM DA MUTANENSA)

126. Manyan mutane na mutanen Fir'auna sukace (dashi,) "Yanzu kuwa barin Musa za kayi da mutanensa donsuyi barna a bayan ƙasa (da kira izuwa saɓa maka, yayi fatali dakai da iyayen -gijinka?" (Ya aikata musu waɗansu gumaka kanana dasuke bauta musu yace shine ubangijinsu tare dasu gumakan don haka yace shine ubangijinsu mafi girma). Yace, "Da san-nu zamu karkashe "ya"yayensu (waɗanda aka haifa,) zamu wanzar da matayen su, (tarnfar yadda mukayi musu tun gaba). Haƙiƙa mu masu rinjaye ne a kansu". (Sukayi musu haka ɗin kuwa sai Bani - Isra'ila suka kai kara).
127. Annabi Musa (Alaihissalam) ya faɗa ga mutanensa, "Ku nemi taimako da Allah ku daure (bisa cutarsu). Haƙiƙa ƙasa dai ta Allah ce yana gadar da ita ga wanda yaga dama daga bayinsa, kyakkyawan ƙarshe ya tabbata ga masu tsoron Allah".
128. Sukace, "An cuce mu tun gaban zuwanka da bayan kazo mana". Sai yace, "Ina kaunar Ubangijinku ya halakar da aduwanku ya mayar daku, mana yansu a cikin ƙasa, ya duba ƙaƙa zaku aikata". a cikinta

(SAKAMAKON MASU SABO A DUNIYA)

129. Haƙiƙa mun kama ali -Fir'auna da fari da tauyewa na "ya"yan itaciya donsu wata kila sa wa'azantu.

فَإِذَا جَآءَتْهُمُ ٱلْحَسَنَةُ قَالُواْ لَنَا هَٰذِهِۦ ۖ وَإِن تُصِبْهُمْ سَيِّئَةٌ
يَطَّيَّرُواْ بِمُوسَىٰ وَمَن مَّعَهُۥٓ ۗ أَلَآ إِنَّمَا طَٰٓئِرُهُمْ عِندَ ٱللَّهِ
وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿130﴾ ۞ وَقَالُواْ مَهْمَا تَأْتِنَا بِهِۦ
مِنْ ءَايَةٍ لِّتَسْحَرَنَا بِهَا فَمَا نَحْنُ لَكَ بِمُؤْمِنِينَ ﴿131﴾ فَأَرْسَلْنَا
عَلَيْهِمُ ٱلطُّوفَانَ وَٱلْجَرَادَ وَٱلْقُمَّلَ وَٱلضَّفَادِعَ وَٱلدَّمَ
ءَايَٰتٍ مُّفَصَّلَٰتٍ فَٱسْتَكْبَرُواْ وَكَانُواْ قَوْمًا مُّجْرِمِينَ ﴿132﴾
وَلَمَّا وَقَعَ عَلَيْهِمُ ٱلرِّجْزُ قَالُواْ يَٰمُوسَى ٱدْعُ لَنَا رَبَّكَ
بِمَا عَهِدَ عِندَكَ ۖ لَئِن كَشَفْتَ عَنَّا ٱلرِّجْزَ لَنُؤْمِنَنَّ لَكَ
وَلَنُرْسِلَنَّ مَعَكَ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ﴿133﴾ فَلَمَّا كَشَفْنَا عَنْهُمُ ٱلرِّجْزَ
إِلَىٰٓ أَجَلٍ هُم بَٰلِغُوهُ إِذَا هُمْ يَنكُثُونَ ﴿134﴾ فَٱنتَقَمْنَا مِنْهُمْ
فَأَغْرَقْنَٰهُمْ فِى ٱلْيَمِّ بِأَنَّهُمْ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَكَانُواْ عَنْهَا غَٰفِلِينَ ﴿135﴾
وَأَوْرَثْنَا ٱلْقَوْمَ ٱلَّذِينَ كَانُواْ يُسْتَضْعَفُونَ مَشَٰرِقَ ٱلْأَرْضِ
وَمَغَٰرِبَهَا ٱلَّتِى بَٰرَكْنَا فِيهَا ۖ وَتَمَّتْ كَلِمَتُ رَبِّكَ
ٱلْحُسْنَىٰ عَلَىٰ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ﴿136﴾ بِمَا صَبَرُواْ ۖ وَدَمَّرْنَا مَا كَانَ
يَصْنَعُ فِرْعَوْنُ وَقَوْمُهُۥ وَمَا كَانُواْ يَعْرِشُونَ ﴿137﴾

ثمن

130. Yayin da ni'ima da wadata tazo musu sai Sukace, "Wannan ai tamu ce". (Basuyi godiya a kanta ba). Idan kuma wahala ta samesu (fari da bala'i,) sai suyi shu'umi da Annabi Musa (Alaihissalam) da waɗanda suke tare dashi (na muminai). To, jama'a dahir dai wannan shu'umin nan nasu yana ga Allah sai dai yawaicinsu basu san (daga Allah yake ba).

131. Sukace, (da Annabi Musa Alaihissalam,) "Kome kazo mana dashi na daga aya donka tsafance mu da ita, mu bazamu gaskata don kai ba".

132. (Sai yayi musu mugunyar addu'a,) sai muka sako kunzumin ruwa a kansu, (yake shiga dakunansu ya sadu izuwa maƙogwaron waɗanda ke zaune kwana bakwai,) da kwar kwata (ta cinye hatsinsu da "ya"yan itaciyarsu kwana bakwai,) da hasu da kwaɗi da jini (a cikin ruwansu). Ayoyi ababen rarrabewa sukayi girman kai (ga buran imani,) sun kasance mutane ne ma'abuta Laifi.

(AKIBAR KAFIRCI DA SABA ALKAWARI)

133. Yayin da azabata auku a kansu, sukace "Ya Musa ka roƙi Ubangijinka garemu, saboda abinda ya alƙawarta gareka (na yaye azaba idan mun bada gaskiya). Wallahi in ka yaye azaba ga buranmu, Lalle zamu gaskatada Allah don ka, Lalle zamu saki Bani - Isra'ila tareda kai.

134. Yayin da muka yaye azaba ga buran su (saboda addu'ar Anna-bi Musa Alaihissalam) izuwa ajali da zasu kai izuwa gareshi, kumfa sai gasu suna warwarewar alƙawarin.

135. Sai mukayi azaba garesu, muka nitsar dasu a cikin Bahar - Maliya, Saboda kasance warsu sun ƙaryata ayoyinmu, sun zama marabkana ga buran tu.

(WANI ABU NA DAGA NI'IMOMIN ALLAH A BISA BANI - ISRA'ILA)

136. Muka gada wa mutanen nan da ake ganin raunin su mahudar rana da mafaɗarta, wacce mukayi albarka a cikinta (da ruwa da itatuwa, da yawan Annabawa iTace Sham). kalmomin Ubangijinka mafi kyau ta cika (iTace muna nufin mu yi baiwa ga waɗanda ake ganin rauninsu a bisa Bani - Isra'ila).

137. Saboda juriyar su ga cutar magautansu muka rugurguza abinda Fir'auna ya aikatada mutanensa na sha'anin noma da abinda suke ɗaukakawa na gine -gine.

(WANI ABU HAR YAU NA DAGA NI'IMOMIN ALLAH A BISA BANI - ISRA'ILA DA KUMA ADA'A DA SUKAYI WA ALLAH)

وَجَٰوَزۡنَا بِبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱلۡبَحۡرَ فَأَتَوۡاْ عَلَىٰ قَوۡمٖ يَعۡكُفُونَ
عَلَىٰٓ أَصۡنَامٖ لَّهُمۡۚ قَالُواْ يَٰمُوسَى ٱجۡعَل لَّنَآ إِلَٰهٗا كَمَا لَهُمۡ
ءَالِهَةٞۚ قَالَ إِنَّكُمۡ قَوۡمٞ تَجۡهَلُونَ ﴿138﴾ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ مُتَبَّرٞ مَّا هُمۡ فِيهِ
وَبَٰطِلٞ مَّا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ﴿139﴾ قَالَ أَغَيۡرَ ٱللَّهِ أَبۡغِيكُمۡ
إِلَٰهٗا وَهُوَ فَضَّلَكُمۡ عَلَى ٱلۡعَٰلَمِينَ ﴿140﴾ وَإِذۡ أَنجَيۡنَٰكُم
مِّنۡ ءَالِ فِرۡعَوۡنَ يَسُومُونَكُمۡ سُوٓءَ ٱلۡعَذَابِ يُقَتِّلُونَ
أَبۡنَآءَكُمۡ وَيَسۡتَحۡيُونَ نِسَآءَكُمۡۚ وَفِي ذَٰلِكُم بَلَآءٞ
مِّن رَّبِّكُمۡ عَظِيمٞ ﴿141﴾ ۞ وَوَٰعَدۡنَا مُوسَىٰ ثَلَٰثِينَ لَيۡلَةٗ
وَأَتۡمَمۡنَٰهَا بِعَشۡرٖ فَتَمَّ مِيقَٰتُ رَبِّهِۦٓ أَرۡبَعِينَ لَيۡلَةٗۚ
وَقَالَ مُوسَىٰ لِأَخِيهِ هَٰرُونَ ٱخۡلُفۡنِي فِي قَوۡمِي وَأَصۡلِحۡ
وَلَا تَتَّبِعۡ سَبِيلَ ٱلۡمُفۡسِدِينَ ﴿142﴾ وَلَمَّا جَآءَ مُوسَىٰ لِمِيقَٰتِنَا
وَكَلَّمَهُۥ رَبُّهُۥ قَالَ رَبِّ أَرِنِيٓ أَنظُرۡ إِلَيۡكَۚ قَالَ لَن تَرَىٰنِي وَلَٰكِنِ ٱنظُرۡ
إِلَى ٱلۡجَبَلِ فَإِنِ ٱسۡتَقَرَّ مَكَانَهُۥ فَسَوۡفَ تَرَىٰنِيۚ فَلَمَّا تَجَلَّىٰ رَبُّهُۥ
لِلۡجَبَلِ جَعَلَهُۥ دَكّٗا وَخَرَّ مُوسَىٰ صَعِقٗاۚ فَلَمَّآ أَفَاقَ
قَالَ سُبۡحَٰنَكَ تُبۡتُ إِلَيۡكَ وَأَنَا۠ أَوَّلُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ﴿143﴾

رُبع

138. Muka ƙetareda Bani - Isara'ila, suka shuɗe bisa waɗansu mutane dasuke dukufa bisa bautar wasu gumaka nasu. Sukace, "Ya Musa sanya mana gunki da zamu bauta masa tamfar dasuke da gumaka". Yace, "Haƙiƙa ku mutane ne jahilai. (kun yi wa Allah ada'a bisa ni'imomin daya gudanar a gareku saboda wannan magana taku mummuna!).

139. "Ai waɗannan mutane ba shakka abinda suke ciki halakakke ne, abinda suke aikatawa kuma na banza ne".

140. Yace, "ƙaƙa zan nema muku wanin Ubangiji abin bautawa, alhali shine yafifita ku a kan talikai?

141. "Ku tuna zamanin daya tserar daku ,daga Fir'auna da mutanensa da suka ɗanɗana muku kuɗa ta azabasuna kashe "ya"yankumaza suna wanzar da matayen ku. A cikin wancananku akwai jarraba maigirma daga Ubangijinku. (Ba kwa wa'azantu bakutuba ga buran wannan mummunar magana daku ,ke faɗa)".

(GANIN ALLAH DA SAUKAR ATTAURA)

142. Munyi wa Annabi Musa (Alaihissalam) alƙawarin kwana talatin, (zamuyi zance dashi yayin cikarsu, muka umarce shiya azumce su shine Zulƙa'ada, ya azumce su yayin dayagama, sai yayi as'waki saboda bashin bakin sa, sai Ubangiji ya umarce shi da ƙara kwana goma saboda yayi zance dashi alhali akwai wannan bashi a bakinsa, kamar yadda Ubangiji yace, "Muka cikatada kwana goma na Zulhajji Lokacin da Ubangi-jinsa yayi alƙarwari zai zance dashiya cika,) sai Annabi Musa ya faɗa ga ɗan'uwansa Annabi Haruna (Alaihissalam, yayin tafiyar sa izuwa dutse don gana wa da Allah,) "Maye min a cikin mutanena ka gyara (al'amarinsu) kadaka bi hanyar mabarnata".

143. Yayin da Annabi Musa (Alaihissalam) ya je a Lokacin da mukayi zamuyi zance dashi a cikinsa, Ubangijinsa yayi zance dashi (bada wasiɗar Mala'ika ba, yaji zancen Allah ta kowace jiha sai yayi bege izuwa ganin Ubangiji. Sai yace "Ubangiji nuna min kanka in dube ka". Sai Ubangiji yace, "Bazaka iyaganina ba" (Mun gode wa Allah a bisa amsawa da aka bashi da wannan siga da bai ce dashi ba a ganina ba,) sai dai yi duba izuwa dutse, (wanda yafi ka ƙarfi) to, idan ya tabbata a gurinsa, to, da sannu ka ganni, (in bai tabbata ba bazaka iyaganina ba)". Yayin da Ubangijinsa ya bayyana ga dutse (wato gwargwadon gaba ɗaya ta ɗankuri na haskensa, tamfar yadda aka faɗa a cikin Hadisin Hakimu) Saiya maidashi dandaƙaƙƙe, Annabi Musa ya faɗi sumamme (saboda tsoron abinda yagani). Yayin daya farka, sai yace "Tsarki ya tabbata gareka! Na tuba gareka, daga roƙon abinda baka umarce ni dashi ba). Nine farkon muminui a zamanina".

قَالَ يَٰمُوسَىٰٓ إِنِّي ٱصۡطَفَيۡتُكَ عَلَى ٱلنَّاسِ بِرِسَٰلَٰتِي وَبِكَلَٰمِي
فَخُذۡ مَآ ءَاتَيۡتُكَ وَكُن مِّنَ ٱلشَّٰكِرِينَ (144) وَكَتَبۡنَا لَهُۥ
فِي ٱلۡأَلۡوَاحِ مِن كُلِّ شَيۡءٖ مَّوۡعِظَةٗ وَتَفۡصِيلٗا لِّكُلِّ شَيۡءٖ
فَخُذۡهَا بِقُوَّةٖ وَأۡمُرۡ قَوۡمَكَ يَأۡخُذُواْ بِأَحۡسَنِهَاۚ سَأُوْرِيكُمۡ
دَارَ ٱلۡفَٰسِقِينَ (145) سَأَصۡرِفُ عَنۡ ءَايَٰتِيَ ٱلَّذِينَ يَتَكَبَّرُونَ
فِي ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَإِن يَرَوۡاْ كُلَّ ءَايَةٖ لَّا يُؤۡمِنُواْ بِهَا
وَإِن يَرَوۡاْ سَبِيلَ ٱلرُّشۡدِ لَا يَتَّخِذُوهُ سَبِيلٗا وَإِن يَرَوۡاْ سَبِيلَ
ٱلۡغَيِّ يَتَّخِذُوهُ سَبِيلٗاۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا
وَكَانُواْ عَنۡهَا غَٰفِلِينَ (146) وَٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا
وَلِقَآءِ ٱلۡأٓخِرَةِ حَبِطَتۡ أَعۡمَٰلُهُمۡۚ هَلۡ يُجۡزَوۡنَ إِلَّا مَا كَانُواْ
ثمن
يَعۡمَلُونَ (147) * وَٱتَّخَذَ قَوۡمُ مُوسَىٰ مِنۢ بَعۡدِهِۦ مِنۡ حُلِيِّهِمۡ
عِجۡلٗا جَسَدٗا لَّهُۥ خُوَارٌۚ أَلَمۡ يَرَوۡاْ أَنَّهُۥ لَا يُكَلِّمُهُمۡ وَلَا يَهۡدِيهِمۡ
سَبِيلًاۘ ٱتَّخَذُوهُ وَكَانُواْ ظَٰلِمِينَ (148) وَلَمَّا سُقِطَ
فِيٓ أَيۡدِيهِمۡ وَرَأَوۡاْ أَنَّهُمۡ قَدۡ ضَلُّواْ قَالُواْ لَئِن لَّمۡ يَرۡحَمۡنَا
رَبُّنَا وَيَغۡفِرۡ لَنَا لَنَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ (149)

144. Ubangiji yace, "Ya Musa, haƙiƙa ni na zaɓe ka a kan mutanen zamanin ka da aikena da zancena. Ka riƙi abinda na baka (na daga falala) ka zamo daga cikin masu godiya (da ni'imomina).

145. Muka rubuta masa a cikin Allunan Attaura (na magaryar aljanna allo bakwai ko goma) daga kowane abu (da ake bukata a gareshi na addini,) gargaɗi da cikakken bayani na kowane abu, mukace (dashi) "Riƙe su da ƙarfi ka umarci mutanenka suyi riƙo da mafi kyanta, da sannu zan nuna muku gidan fasiƙai, (Fir'auna da mutanensa don kuyi izna dasu)".

(ABINDA YAKE SABAUTA KAFIRCI GALIBAN)

146. Da sannu zan juyar ga buran ayoyina, (wato al'ajuban ikona,) zan juyar da masu girman kai a cikin ƙasa bada gaskiya ba, in taɓar dasu baza suyi tunani a cikinta ba, in sun ga kowace aya bazasu bada gaskiya da ita ba, in sun ga hanyar shiriya bazasu rike ta hanya ba. (Tamfar yadda yake shine halin da muke ciki a yau, Inna Lillahi Wa Inna Ilaihi Raji'una, wannan dalili da Ubangiji ya faɗa shine ya kawo halaka a cikin wannan duniya bakiɗaya). In sun ga hanyar ɓata saisu rike ta hanya. Wannan juyarwa saboda haƙiƙa su sun ƙaryata ne da ayoyinmu sunzamo marabkana ga buran su.

147. Waɗanda suka ƙaryata Ayoyinmu da Tashin alƙiyama, ayyukansu nagari (kamar sadaka da sadar da zumunta) sun Lalace. (Baza a basu Lada a kai ba saboda rashin Musulunci garesu). Ba a saka musu kome sai abinda suka aikata.

(BA'ALIN AYYUKANSU BAYAN FAKUWAR ANNABI MUSA ALAIHISSALAM GA BURAN SU)

148. Mutanen Annabi Musa (Alaihissalam) suka riki ɗan Maraƙi abin bautawa bayan tafiyarsa izuwa gana wa da Allah, daga kayan adonsu (wanda suka aro daga mutanen Fir'auna saboda wani angwanci daza suyi.Shi ɗan Maraƙin nan jiki ne, wato nama da jini, yana gunji saboda turɓaya wacce Samiri ya danka daga kofaton goɗiyar Jibrilu Alaihissalam, ya zuba a cikin bakin ta sai rayuwa ta nasu a cikinsa). Shin basa ganin cewa shi ba yayi musu magana, baya shiriyar dasu hanya. ƙaƙa zasu riƙe shi ubangiji? Sun riƙe shi ubangiji sun zamo azzalumai (saboda wannan riƙo).

149. Yayin da suka ciji hannuwansu (wato yan yatsum su) nadama a bisa bautar dan maraki, suka tabbatacewa su sun halaka, (bayan komowar Annabi Musa Alaihissalam,) sai Sukace, "Wallahi in Ubangijinmu bai jiƙanmu ba, bai yi gafara garemu ba, Lalle zamu zamo cikin taɓaɓɓu".

(ABINDA YA TABBATA GA ANNABI MUSA ALAI-HISSALAM BAYAN KOMOWARSA)

وَلَمَّا رَجَعَ مُوسَىٰٓ إِلَىٰ قَوْمِهِۦ غَضْبَٰنَ أَسِفًا قَالَ بِئْسَمَا خَلَفْتُمُونِي
مِنۢ بَعْدِيٓ أَعَجِلْتُمْ أَمْرَ رَبِّكُمْ وَأَلْقَى ٱلْأَلْوَاحَ وَأَخَذَ بِرَأْسِ
أَخِيهِ يَجُرُّهُۥٓ إِلَيْهِ قَالَ ٱبْنَ أُمَّ إِنَّ ٱلْقَوْمَ ٱسْتَضْعَفُونِي وَكَادُواْ
يَقْتُلُونَنِي فَلَا تُشْمِتْ بِيَ ٱلْأَعْدَآءَ وَلَا تَجْعَلْنِي مَعَ ٱلْقَوْمِ
ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿150﴾ قَالَ رَبِّ ٱغْفِرْ لِي وَلِأَخِي وَأَدْخِلْنَا فِي رَحْمَتِكَ
وَأَنتَ أَرْحَمُ ٱلرَّٰحِمِينَ ﴿151﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ ٱلْعِجْلَ
سَيَنَالُهُمْ غَضَبٌ مِّن رَّبِّهِمْ وَذِلَّةٌ فِي ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا وَكَذَٰلِكَ
نَجْزِي ٱلْمُفْتَرِينَ ﴿152﴾ وَٱلَّذِينَ عَمِلُواْ ٱلسَّيِّـَٔاتِ ثُمَّ تَابُواْ
مِنۢ بَعْدِهَا وَءَامَنُوٓاْ إِنَّ رَبَّكَ مِنۢ بَعْدِهَا لَغَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿153﴾
وَلَمَّا سَكَتَ عَن مُّوسَى ٱلْغَضَبُ أَخَذَ ٱلْأَلْوَاحَ وَفِي نُسْخَتِهَا
هُدًى وَرَحْمَةٌ لِّلَّذِينَ هُمْ لِرَبِّهِمْ يَرْهَبُونَ ﴿154﴾ وَٱخْتَارَ مُوسَىٰ
قَوْمَهُۥ سَبْعِينَ رَجُلًا لِّمِيقَٰتِنَا فَلَمَّآ أَخَذَتْهُمُ ٱلرَّجْفَةُ
قَالَ رَبِّ لَوْ شِئْتَ أَهْلَكْتَهُم مِّن قَبْلُ وَإِيَّٰيَ أَتُهْلِكُنَا بِمَا فَعَلَ
ٱلسُّفَهَآءُ مِنَّآ إِنْ هِيَ إِلَّا فِتْنَتُكَ تُضِلُّ بِهَا مَن تَشَآءُ وَتَهْدِي مَن تَشَآءُ
أَنتَ وَلِيُّنَا فَٱغْفِرْ لَنَا وَٱرْحَمْنَا وَأَنتَ خَيْرُ ٱلْغَٰفِرِينَ ﴿155﴾

150. Yayin da Annabi Musa (Alaihissalam) yakomo izuwa mutanensa yana mai fushi dasu, yana mai harzuƙa, sai yace (dasu,) "Tir! da wannan mayewa da kukayi min bayana. Shin kun gaggauci al'amarin Ubangijinku ne? Ya zubar da allunan Attaura (saboda fushin dayayi don an saɓa al'amarin Allah, suka karairaye,) ya kama kan ɗan'uwansa Haruna (wato gashin kansa da hannun dama, ge-munsa da hannun hagu) yana fizgarsa izuwa gareshi, (don fushi). Yace da Annabi Musa "Ya ɗan'uwana haƙiƙa mutanen nan sun ga raunina ne sun kusa su kashe ni. Kadaka daraitar da magautada ni, (ma'ana kadaka wulakanta ni magauta suyi dariya,) kadaka sanya ni tareda mutane azzalumai (masu bautar ɗan maraƙi)".

151. Yace, "Ubangiji gafarta min (abinda nayi wa ɗan'uwana) kuma kayi masa gafara (shi
ɗan'uwan nan nawa) ka shigar da mu cikin rahamarka. Kaine mafi jinƙan masu jinƙai. (Ya tara ɗan'uwansa a cikin addu'a don rarrashi da ije ganganko)".

(SAKAMAKON AZZALUMAI)

152. Haƙiƙa waɗanda suka bautawa ɗan maraƙi da sannu azabadaga Ubangijinsu zata samesu da wulakanci a cikin rayuwar duniya. (Akayi musu azabada umarnin su da kashe kawukansu) a ka buga wulakanci a kansu har izuwa Ranar Alƙiyama, (ga mudai muna fama dasu har yau saboda shu'umin daya same mu na wajen sake da dokokin Alƙur'ani, Allah yabamu galaba a kansu Amin). Tamfar da muka saka musu haka nan muke sakawa masu ƙirƙirar ƙarya bisa Allah.

153. Waɗanda suka aikata miyagun ayyuka sannan suka tuba bayan su suka bada gaskiya, haƙiƙa Ubangijinka bayan tuban nan mai gafara ne mai jinƙai.

(ƘARSHEN ƘISSAR BAUTAR DAN MARAƘI)

154. Yayin da fushiya nutsu ga buran Annabi Musa (Alaihissalam, ai yayin daya huce yakomo cikin natsuwa) saiya ɗebi allunan nan. A cikin rubutunsu akwai shiriya da rahama ga waɗanda suke yin gezau saboda Ubangijinsu.

(ABINDA YA TABBATA GA ANNABI MUSA ALAIHISSALAM TSATTSAKIN GANAWA)

155. Annabi Musa (Alai-hissalam) ya zaɓi mutane saba'in (daga waɗanda basu bautawa ɗan maraƙi ba) daga mutanensa (da umarnin Ubangiji) don Lokaci (wanda akayi masa alƙawari dayazo dasu a cikinsa donsuyi hanzari daga bautar "yan'uwansu ga ɗan maraƙi, yafita dasu). To, yayin da girgizata kama su (Ibn Abbas yace don basu ware waje ɗayabane daga masu bautar gumakan kuma har yau basune mutanen da suka roƙi su ga Allah ƙarara ba,) sai Annabi Musa Alai-hissalam yace, (da Ubangiji) "Daka ga dama daka halakar dasu tun gaban fitowa ta dasu, (don Bani - Isra'ila su gani kadasu tuhunce ni da ƙisan su). Ubangiji kadaka halakar da mu saboda abinda wawayenmu suka aikata. Wannan fitina wacce ta auku daga wawayenmu bata kasance ba sai jarrabar ka kana ɓatar da wandaka ga dama da ita, kana shiriyar da wandaka ga dama. Kaine majiɓincin al'amurranmu, sai ka gafarce mu, ka yafe mu, Kaine fiyayyen masu gafartawa".

ربع

۞ وَاكْتُبْ لَنَا فِي هَٰذِهِ الدُّنْيَا حَسَنَةً وَفِي الْآخِرَةِ إِنَّا هُدْنَا
إِلَيْكَ قَالَ عَذَابِي أُصِيبُ بِهِ مَنْ أَشَاءُ وَرَحْمَتِي
وَسِعَتْ كُلَّ شَيْءٍ فَسَأَكْتُبُهَا لِلَّذِينَ يَتَّقُونَ
وَيُؤْتُونَ الزَّكَاةَ وَالَّذِينَ هُمْ بِآيَاتِنَا يُؤْمِنُونَ ﴿156﴾
الَّذِينَ يَتَّبِعُونَ الرَّسُولَ النَّبِيءَ الْأُمِّيَّ الَّذِي يَجِدُونَهُ مَكْتُوبًا
عِنْدَهُمْ فِي التَّوْرَاةِ وَالْإِنْجِيلِ يَأْمُرُهُمْ بِالْمَعْرُوفِ وَيَنْهَاهُمْ
عَنِ الْمُنْكَرِ وَيُحِلُّ لَهُمُ الطَّيِّبَاتِ وَيُحَرِّمُ عَلَيْهِمُ الْخَبَائِثَ
وَيَضَعُ عَنْهُمْ إِصْرَهُمْ وَالْأَغْلَالَ الَّتِي كَانَتْ عَلَيْهِمْ
فَالَّذِينَ آمَنُوا بِهِ وَعَزَّرُوهُ وَنَصَرُوهُ وَاتَّبَعُوا النُّورَ
الَّذِي أُنْزِلَ مَعَهُ أُولَٰئِكَ هُمُ الْمُفْلِحُونَ ﴿157﴾ قُلْ يَا أَيُّهَا النَّاسُ
إِنِّي رَسُولُ اللَّهِ إِلَيْكُمْ جَمِيعًا الَّذِي لَهُ مُلْكُ
السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ يُحْيِي وَيُمِيتُ
فَآمِنُوا بِاللَّهِ وَرَسُولِهِ النَّبِيءِ الْأُمِّيِّ الَّذِي يُؤْمِنُ بِاللَّهِ
وَكَلِمَاتِهِ وَاتَّبِعُوهُ لَعَلَّكُمْ تَهْتَدُونَ ﴿158﴾ وَمِنْ
قَوْمِ مُوسَىٰ أُمَّةٌ يَهْدُونَ بِالْحَقِّ وَبِهِ يَعْدِلُونَ ﴿159﴾

156. Ubangiji ka rubuta mana kyakkyawa a wannan duniya a Lahira ka rubuta mana kyakkyawa, haƙiƙa mu mun tuba izuwa gareka, Ubangiji yace, "Azabata ina samun wandana ga dama da ita, rahamata ta yalwaci komai (a duniya). Da sannu zan rubuta ta (a Lahira) ga waɗanda suke jin tsorona, suke bada zakka da waɗanda suka bada gaskiya da ayoyinmu.

(ANNABI MUHAMMADU TSIRAN ALLAH DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARESHI DA AIKENSA DA WAƊANDA SUKA BADA GASKIYA DASHI) SUNE HAƘIƘAR MARA BAUTA.

157. Waɗanda suke bin Manzo, Annabi maita kama da wahayi (tsiran Allah da amincinsa ya tabbata a gareshi,) wanda suke samunsa a rubuce a cikin Attaura da injila (dasunansa da kamarsa,) yana umarninsu da abin sani a shari'a, yana hana su ga barin aikin munkari, yana halatta musu halal, yana haramta musu miyagun al'amura (wato dukkan abin haramtawa,) yana saryar da nauyi ga buran su, da tsanance tsanance wacce ta kasance a kansu (kamar kashe kai a cikin tubadayanke gurbin najasa). Waɗanda suka bada gaskiya daga cikinsu, suka darajanta shi, suka taimake shi, sukabi haske wanda aka saukar tare dashi (Alƙur'ani,) waɗannan sune haƙiƙa marabauta.

(ANNABI MUHAMMADU TSIRAN ALLAH DA AMINCINSA YA TABBATA GARESHI DA GAMAWAR AIKENSA IZUWA DUK DUNIYA)

158. Cene (dasu) "Yaku waɗannan mutane ni jakadan Allah ne zuwa gareku bakiɗaya, wanda mulkin sammai da ƙassaiya tabbata a gareshi, ba abin bautawa da gaskiya sai shi. Shine mai rayawa mai kashewa, ku bada gaskiya da Allah da manzonsa Annabi wanda bai koyi rubutu da karatu ba, (sai wahayi,) wanda ya bada.gaskiya da Allah da kalmominsa (Alƙur'ani ke nan) kubi shi don ku shiriya.

(WANI ABU NA DAGA NI'IMOMIN ALLAH A BISA BANI - ISRA'ILA)

159. Akwai al'umma daga mutanen Annabi Musa (Alaihissalam) dasuke shiryar da mutane izuwa gaskiya da gaskiya, kuma suke adalci dashi (a cikin hukunci)

وَقَطَّعْنَٰهُمُ ٱثْنَتَيْ عَشْرَةَ أَسْبَاطًا أُمَمًاۚ وَأَوْحَيْنَآ إِلَىٰ
مُوسَىٰٓ إِذِ ٱسْتَسْقَىٰهُ قَوْمُهُۥٓ أَنِ ٱضْرِب بِّعَصَاكَ ٱلْحَجَرَۖ
فَٱنۢبَجَسَتْ مِنْهُ ٱثْنَتَا عَشْرَةَ عَيْنًاۖ قَدْ عَلِمَ كُلُّ أُنَاسٍ
مَّشْرَبَهُمْۚ وَظَلَّلْنَا عَلَيْهِمُ ٱلْغَمَٰمَ وَأَنزَلْنَا عَلَيْهِمُ
ٱلْمَنَّ وَٱلسَّلْوَىٰۖ كُلُواْ مِن طَيِّبَٰتِ مَا رَزَقْنَٰكُمْۚ
وَمَا ظَلَمُونَا وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمْ يَظْلِمُونَ ﴿160﴾
وَإِذْ قِيلَ لَهُمُ ٱسْكُنُواْ هَٰذِهِ ٱلْقَرْيَةَ وَكُلُواْ مِنْهَا حَيْثُ
شِئْتُمْ وَقُولُواْ حِطَّةٌ وَٱدْخُلُواْ ٱلْبَابَ سُجَّدًا
تُغْفَرْ لَكُمْ خَطِيٓـَٰتُكُمْۚ سَنَزِيدُ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿161﴾ فَبَدَّلَ
ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مِنْهُمْ قَوْلًا غَيْرَ ٱلَّذِي قِيلَ لَهُمْ
فَأَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ رِجْزًا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ بِمَا كَانُواْ
يَظْلِمُونَ ﴿162﴾ ۞ وَسْـَٔلْهُمْ عَنِ ٱلْقَرْيَةِ ٱلَّتِي كَانَتْ حَاضِرَةَ ثمن
ٱلْبَحْرِ إِذْ يَعْدُونَ فِي ٱلسَّبْتِ إِذْ تَأْتِيهِمْ حِيتَانُهُمْ
يَوْمَ سَبْتِهِمْ شُرَّعًا وَيَوْمَ لَا يَسْبِتُونَ لَا تَأْتِيهِمْۚ
كَذَٰلِكَ نَبْلُوهُم بِمَا كَانُواْ يَفْسُقُونَ ﴿163﴾

160. Kuma muka rarrabasu kaɓila goma sha biyu, al'umma daban daban. Muka aiko izuwa Annabi Musa zamanin da mutanensa suka nemi sha da ruwa (a cikin dimuwa, muka aiko) cewa doki dutse da sandarka. (Ya doke shi) sai idaniya goma sha biyu ta ɓarke daga gareshi, (gwargwadon adadin waɗannan ƙabilu guda goma sha biyu). Haƙiƙa kowace ƙabila daga cikinsu ta san wajen shan ruwanta. Muka inuwance su da girgije a cikin ɗimuwa (saboda zafin rana,) muka saukar da Darɓa da Danshila a garesu. Mukace dasu "Kuci daga daɗaɗan abinda muka azurta muku". Basu zalunce mu ba sai dai kansu kaɗai suke zalunta.

161. Ka ambata zamanin da mukace (dasu) "Ku zauna a wannan alƙarya (Baitul - Maƙadisi) Kuci daga gareta (duk abinda kuke so). Ku ce, "Abinda muke bara saryar da zunubanmu." Ku shiga ƙofar wannan alƙarYakuna masu sunkuyar da kawunanku, a gafarta muku kurakuran ku. Da sannu zamu ƙarawa masu kyakkyawan aiki sakamako".

162. Sai waɗanda sukayi zalunci daga garesu suka musanya magana suka faɗi wanin abinda akace dasu faɗa, (Sukace, "ƙwaya a cikin gashi" suka shiga suna jan gindi). Sai muka aiko musu azabadaga sama saboda kasancewarsu azzalumai.

(AƘIBAR MASU SABAWA DA RABAUTAR MASU UMARNI DA ABIN SANI A SHARI'A)

163. Tambaye su (Ya Annabi tsiran Allah da amincinsa su tabbata a gareka don muzantawa garesu) ga alƙarya wacce ta kasance a gefen kogi (kogin kulzumu iTace Ailatu. Me ya auku ga mutanenta,) zamanin da sukayi shisshigi zamanin da sukayi sun kifi a cikin ranar Asabar (wanda aka umarce su da barinsa). Zamanin da kifaye suke zuwa musu a ranar Asabacin, suna masu banbaro a kan ruwa, a ranar da ba Asabar bakuwa basa zuwa musu, (don jarraba daga Allah). Haka nan muke jarrabarsu Don sun , kasance fasiƙai.

وَإِذْ قَالَتُ اُمَّةٞ مِّنْهُمْ لِمَ تَعِظُونَ قَوْمًا اَ۬للَّهُ مُهْلِكُهُمُۥٓ أَوْ مُعَذِّبُهُمْ
عَذَابًا شَدِيدًا قَالُواْ مَعْذِرَةٌ اِلَىٰ رَبِّكُمْ وَلَعَلَّهُمْ يَتَّقُونَ ﴿164﴾
فَلَمَّا نَسُواْ مَا ذُكِّرُواْ بِهِۦٓ أَنجَيْنَا اَلذِينَ يَنْهَوْنَ عَنِ
اِ۬لسُّوٓءِ وَأَخَذْنَا اَلذِينَ ظَلَمُواْ بِعَذَابِۢ بِيسٍ بِمَا كَانُواْ
يَفْسُقُونَ ﴿165﴾ فَلَمَّا عَتَوْاْ عَن مَّا نُهُواْ عَنْهُ قُلْنَا لَهُمْ كُونُواْ
قِرَدَةً خَٰسِـِٔينَ ﴿166﴾ وَإِذْ تَأَذَّنَ رَبُّكَ لَيَبْعَثَنَّ عَلَيْهِمُۥٓ إِلَىٰ يَوْمِ
اِ۬لْقِيَٰمَةِ مَنْ يَسُومُهُمْ سُوٓءَ اَ۬لْعَذَابِ إِنَّ رَبَّكَ لَسَرِيعُ اُ۬لْعِقَابِ
وَإِنَّهُۥ لَغَفُورٞ رَّحِيمٞ ﴿167﴾ وَقَطَّعْنَٰهُمْ فِي اِ۬لْأَرْضِ أُمَمًا مِّنْهُمُ
اُ۬لصَّٰلِحُونَ وَمِنْهُمْ دُونَ ذَٰلِكَ وَبَلَوْنَٰهُم بِالْحَسَنَٰتِ
وَالسَّيِّـَٔاتِ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿168﴾ فَخَلَفَ مِنۢ بَعْدِهِمْ خَلْفٞ
وَرِثُواْ اُ۬لْكِتَٰبَ يَأْخُذُونَ عَرَضَ هَٰذَا اَ۬لْأَدْنَىٰ وَيَقُولُونَ
سَيُغْفَرُ لَنَا وَإِنْ يَّأْتِهِمْ عَرَضٞ مِّثْلُهُۥ يَأْخُذُوهُ أَلَمْ يُؤْخَذْ عَلَيْهِم
مِّيثَٰقُ اُ۬لْكِتَٰبِ أَن لَّا يَقُولُواْ عَلَى اَ۬للَّهِ إِلَّا اَ۬لْحَقَّ وَدَرَسُواْ مَا فِيهِ
وَالدَّارُ اُ۬لْأٓخِرَةُ خَيْرٞ لِّلذِينَ يَتَّقُونَ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿169﴾ وَالذِينَ
يُمَسِّكُونَ بِالْكِتَٰبِ وَأَقَامُواْ اُ۬لصَّلَوٰةَ إِنَّا لَا نُضِيعُ أَجْرَ اَ۬لْمُصْلِحِينَ ﴿170﴾

164. Haka nan zamanin da al'umma daga garesu tace, (wato sune wađanda basuyi su ba, basuyi hani ga wanda yayi su ba). Donme kuke gargađi ga mutane wađanda Allah zai halakar dasu, ko zai azabtar dasu azaba mai tsanani?" Sai Sukace, "Gargađinmu)hanzari izuwa Ubangijinku (don kada a dangana mu izuwa takaitawa a cikin barin hani,) kuma don mutanen nan suji tsoron (yinsu a ranar Asabar)".

165. Yayin da suka mance abinda akayi musu gargađi dashi sai muka tserar da wađanda suke hani ga barin mummunan aiki muka kama wađanda sukayi zalunci da azaba mai tsanani saboda kasancewar su fasiƙai.

166. A yayin da sukayi tsaurin kai ga barin abinda aka hane su ga buransa, sai mukace dasu, "Ku zama birrai wulakantattu".(Suka zama birran).

(HAKA NAN YAHUDAWA,A DUNIYA)

167. Ka ambata musu zamanin da Ubangijinka yace "Lallai zai aiko wandazai đanđana musu kuđarsu (wato mummunar azaba) izuwa Ranar Alƙiyama, da wulaƙanci (da karɓar jiziya. Ya aiko Annabi Sulaiman a kansu abayansa kuma Buhtu - Nassar, ya kashe su ya ribace su yasanyajiziya a kansu, suka dinga bada ita izuwa Maguzawahar izuwa Allah ya aiko manzon Allah tsira da aminci su tabbata gareshi yasanya ta a kansu). Haƙiƙa Ubangijinka mai garajen uƙubane (ga wanda ya sabe shi). Haƙiƙa shi mai yawan gafara ne (ga wanda yabi shi)".

168. Muka rarrabe su a ƙasa daban -daban ƙabila - ƙabila. Akwai managarta daga cikinsu, akwai daga cikinsu koma bayan wan-canenka kafirai ke nan da fasiƙai. Muka jarrabe su da ni'imomi da kuma azaba, donsu komo (gaburan fasiƙanci).

169. To, sai mutanen banza suka maye bayansu, sun gaji Attaura ga iyayensu suna riƙon tarkacen wannan wulaƙantacciyar duniya (halal da haram,) suna cewa, "Da sannu za a gafarta mana abinda muka aikata" in kuma irin wannan tarkace yazo musu saisu sake karɓarsa, gashi kuma ba ayi alƙawarin gafara ga wanda ya dauwama a cikin zunibi a cikin Attaura ba, (kamar yadda mu ma ba ayi anamu alƙur'anin ba). Shin ba a karɓo alƙawarin Littafi bane a kansu cewa kadasu fađa ga Allah sai gaskiya? Sun kuma karanta abinda yake cikinsa (to, donme sukace za ayi musu gafara tareda zarcewar su cikin zunubi?) Gidan Lahira shi yafi ga wađanda suke jin tsoron Allah, shin basayi hankali ba (su fifita ta a kan duniya?)

170. Wađanda suke ƙanƙame Littafi (wato suke riƙe shi riƙon gaskiya daga cikinsu,) suka tsaida sallah, haƙiƙa mu Barna tozarta Ladan masu inganta aiki.

* وَإِذْ نَتَقْنَا ٱلْجَبَلَ فَوْقَهُمْ كَأَنَّهُۥ ظُلَّةٌ وَظَنُّوٓاْ أَنَّهُۥ وَاقِعُۢ بِهِمْ خُذُواْ
مَآ ءَاتَيْنَٰكُم بِقُوَّةٍ وَٱذْكُرُواْ مَا فِيهِ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴿171﴾ وَإِذْ أَخَذَ
رَبُّكَ مِنۢ بَنِىٓ ءَادَمَ مِن ظُهُورِهِمْ ذُرِّيَّٰتِهِمْ وَأَشْهَدَهُمْ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ
أَلَسْتُ بِرَبِّكُمْ قَالُواْ بَلَىٰ شَهِدْنَآ أَن تَقُولُواْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ إِنَّا كُنَّا عَنْ هَٰذَا
غَٰفِلِينَ ﴿172﴾ أَوْ تَقُولُوٓاْ إِنَّمَآ أَشْرَكَ ءَابَآؤُنَا مِن قَبْلُ وَكُنَّا
ذُرِّيَّةً مِّنۢ بَعْدِهِمْ أَفَتُهْلِكُنَا بِمَا فَعَلَ ٱلْمُبْطِلُونَ ﴿173﴾
وَكَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلْءَايَٰتِ وَلَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿174﴾ وَٱتْلُ
عَلَيْهِمْ نَبَأَ ٱلَّذِىٓ ءَاتَيْنَٰهُ ءَايَٰتِنَا فَٱنسَلَخَ مِنْهَا فَأَتْبَعَهُ
ٱلشَّيْطَٰنُ فَكَانَ مِنَ ٱلْغَاوِينَ ﴿175﴾ وَلَوْ شِئْنَا لَرَفَعْنَٰهُ
بِهَا وَلَٰكِنَّهُۥٓ أَخْلَدَ إِلَى ٱلْأَرْضِ وَٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ فَمَثَلُهُۥ
كَمَثَلِ ٱلْكَلْبِ إِن تَحْمِلْ عَلَيْهِ يَلْهَثْ أَوْ تَتْرُكْهُ يَلْهَث
ذَّٰلِكَ مَثَلُ ٱلْقَوْمِ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا فَٱقْصُصِ
ٱلْقَصَصَ لَعَلَّهُمْ يَتَفَكَّرُونَ ﴿176﴾ سَآءَ مَثَلًا ٱلْقَوْمُ ٱلَّذِينَ
كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَأَنفُسَهُمْ كَانُواْ يَظْلِمُونَ ﴿177﴾ مَن يَهْدِ
ٱللَّهُ فَهُوَ ٱلْمُهْتَدِى وَمَن يُضْلِلْ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْخَٰسِرُونَ ﴿178﴾

171. Ka ambata zamanin da muka tunbuko dutse muka ɗagashi burbushinsu kai kace shi rumfa ce suka tabbatacewa shi zai faɗo a kansu, (saboda Allah ya alƙawarta musu faɗowar dutsen nan kansu in basu karɓi hukuncin Attaura ba, sun ƙi ƙarɓa kuwa ne saboda nauyin hukunce - hukunce ne. To, sai suka karɓa. Mukace dasu,) "Ku kama abinda muka bakuda ƙarfi kuyi aiki da abinda yake ciki don ku tsoraci Allah.

(TSOHON ALƘAWARI WANDA AKA RIKA BISA BANI - ADAMA TUN ALAMUZZARRI)

172. Ka ambata zamanin da Ubangijinka yafito da Bani - Adama daga bayayyakin su yafito da zurriyoyinsu, (shine yafitar da sashinsu daga tsatson sashi daga tsatson Annabi Adamu Alai-hissalam, ƙabila bayan ƙabila, irin yadda suke haihuwar juna, kamar kwayar zarra, a guri da ake ce masa Na'amanul - araki, wato Annabi Adamu ya zamo kamar ɗan ɓallan bishiyar.Wannan abu ya afku ranar Arfa,. ya kafa musu dalilai a bisa Allantakarsa, ya shigar da hankali a cikinsu) ya shaidar dasu a bisa kawukansu, (yace) "Shin banine Ubangijinku ba?" Sukace, "Kaine Ubangijinmu! Mun shaidar da wannan," shaidar wannan kuwa, don kadaku ,(kafurai) Ranar Alƙiyama ku ce, Mu mun kasance marabkana ne ga buran wannan Tauhidi, bamu sanshi ba.

173. Koku ce, "Iyayenmu dasuke gabanmune sukayi shirka, mu mun kasance zuriyya bayansu, (mukayi koyi dasu). To, Ubangiji kada kayi mana azabada abinda mabarnata (na iyayenmu) suka aikata.

174. Haka na muke rarrabe ayoyi (tamfar yadda muka bayyana alƙawarin nan donsu Lura da ita,) saboda su koma (ga buran kafircinsu).

(MISALIN MASU ƘARYATA MAN-ZANNI DA MIYAGUN MALAMAI)

175. Karanta a garesu (Ya Muhammadu Sallallahu alaika wasallama,) babbar magana wanda muka bashi ayoyinmu ya tuɓu daga gareta (saboda kafircinsa shine Bal'amu ɗan Ba'ura daga malaman Banu - Isra'ila. Sun nemi yayi mummunar addu'a a kan Annabi Musa Alai-hissalam, suka bashi rashawa yayi addu'ar, saita dinga juyawa a kansu maimakon ya faɗi sharri sai hairi. Harshensa ya zazzago a kan kirjinsa). To, sai shaiɗan) ya riske shi (ya zama ɗanmorin shaiɗan) saboda haka ya zama cikin halakakku.

176. Da mun ga dama da sai mu daukaka shi da ita wannan aya, mukai shi martabar masanan Allah, (shine ayi masa mawafaƙa yayi aiki da ita,) sai dai shi kawai ya zarmu a cikin son duniya yabi son zuciyarsu. Misalinsa kamar kare in kayi ɗauki kansa (da kora da tsawa) sai yayi haki, (da sakin harshensa,) in ka bar shima yayi haki, (sauran dabbobi kuwa ba haka suke ba). Wannan misali shine misalin mutanen dasuke ƙaryata ayoyinmu, sai ka Labarta, Labartawa donsuyi cikakken tunani (su bada gaskiya).

177. Tur dashi misali! misalin waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu kansu kaɗai suka kasance suke zalunta.

(SIFFAR 'YAN WUTA)

178. Wanda Allah ya shirye shi, to, shine kaɗai mai shiriya. Waɗanda Allah ya ɓatar, waɗancananka su kaɗai ne taɓaɓɓu.

ثمن

وَلَقَدْ ذَرَأْنَا لِجَهَنَّمَ كَثِيراً مِّنَ اَلْجِنِّ وَالِانسِ لَهُمْ قُلُوبٌ لَّا يَفْقَهُونَ
بِهَا وَلَهُمْ أَعْيُنٌ لَّا يُبْصِرُونَ بِهَا وَلَهُمْ ءَاذَانٌ لَّا يَسْمَعُونَ بِهَا
أُوْلَٰٓئِكَ كَالْأَنْعَٰمِ بَلْ هُمْ أَضَلُّ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ الْغَٰفِلُونَ ﴿179﴾ * وَلِلَّهِ
الْأَسْمَآءُ الْحُسْنَىٰ فَادْعُوهُ بِهَا وَذَرُوا الَّذِينَ يَلْحَدُونَ فِي أَسْمَٰٓئِهِ
سَيُجْزَوْنَ مَا كَانُوا يَعْمَلُونَ ﴿180﴾ وَمِمَّنْ خَلَقْنَا أُمَّةٌ يَهْدُونَ
بِالْحَقِّ وَبِهِ يَعْدِلُونَ ﴿181﴾ وَالَّذِينَ كَذَّبُوا بِـَٔايَٰتِنَا سَنَسْتَدْرِجُهُم
مِّنْ حَيْثُ لَا يَعْلَمُونَ ﴿182﴾ وَأُمْلِي لَهُمُ إِنَّ كَيْدِي مَتِينٌ ﴿183﴾ أَوَلَمْ
يَتَفَكَّرُوا مَا بِصَاحِبِهِم مِّن جِنَّةٍ إِنْ هُوَ إِلَّا نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿184﴾
أَوَلَمْ يَنظُرُوا فِي مَلَكُوتِ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَمَا خَلَقَ اللَّهُ
مِن شَيْءٍ وَأَنْ عَسَىٰ أَن يَكُونَ قَدِ اقْتَرَبَ أَجَلُهُمْ فَبِأَيِّ حَدِيثٍ
بَعْدَهُ يُؤْمِنُونَ ﴿185﴾ مَن يُضْلِلِ اللَّهُ فَلَا هَادِيَ لَهُ وَنَذَرُهُمْ
فِي طُغْيَٰنِهِمْ يَعْمَهُونَ ﴿186﴾ يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ السَّاعَةِ أَيَّانَ مُرْسَىٰهَا
قُلْ إِنَّمَا عِلْمُهَا عِندَ رَبِّي لَا يُجَلِّيهَا لِوَقْتِهَا إِلَّا هُوَ ثَقُلَتْ فِي السَّمَٰوَٰتِ
وَالْأَرْضِ لَا تَأْتِيكُمُ إِلَّا بَغْتَةً يَسْـَٔلُونَكَ كَأَنَّكَ حَفِيٌّ عَنْهَا
قُلْ إِنَّمَا عِلْمُهَا عِندَ اللَّهِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ النَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿187﴾

179. Hak̃ik̃a mun halicci yawaici na aljannu da mutane don wutar Jahannama. Zukata na garesu basu fahimtar (gaskiya) dasu. ida-nuwa na garesu da basa ganin (dalilan ikon Allah) dasu, kunnuwa na garesu basa jin (gargaɗi) dasu. Waɗancananka kamar dabbobi suke, Kai! su ma sun fi dabbobi ɓata saboda cewa Ita tana neman abindazai amfa neta, tana gudu doga abindazai cuce ta. waɗannan kuwa suna zunduma akan wutada gan-gan Waɗancananka sune hak̃ik̃ar marabkana.

(SUNAYEN UBANGIJI KYAWAWA)

180. Sunannaki kyawawa sun tabbata ga Allah, (guda ɗari ɗaya -babu, waɗanda Hadisi yazo dasu, amma basu ke nan sunannankin Allah ba, an samu waɗansu sunayen ta riwayoyi daban - daban da suka kai wanna adadi ko suka fi, to a hak̃ik̃a dai sunan Allah baya tsaruwa a kan wannan ɗari ɗaya - babu, sai dai mashahuran wato ɗari daya - babu haka suke'a ruwayar Tirmizi ga Abu Hurairata wacce iTace mashahuriya). Ku rok̃e shi dasu ku rabu da waɗanda suke yin kangara a cikin sunannakinsa; (da suka tsago sunannakin gumakansu daga sunannakin Allah, kamar Latu daga Allah, da Uzza daga Azi-zu, Manatu daga Mannanu, ko makamancin haka kamar Lahani cikin hailala ko cikin wani suna daga cikin sunan nakinsa ko sunannakin Manzon sa (S.A.W) kamar Muhammadu ace muhammed). Da sannu za a saka musu (a Lahira) abinda suka kasance suna aikatawa.

(SHIRYAYYUN AL'UMAR MANZON ALLAH DA BATATTU)

181. Akwai al'umma daga cikin halittarmu suna shiryarwa da gaskiya, suna yin adalci da ita.

182. Waɗanda suka karyatada ayoyinmu (Alk̃ur'ani, mutanen Makka da waninsu) da sannu zamuyi musu mak̃ark̃ashiya, mu kama su kaɗan - kaɗan ta inda basu sani ba.

183. Inayi musu talala, hak̃ik̃a kaidina (wato shirina) k̃ak̃k̃arfa ne ba mai iya masa.

184. Yanzu basayi tunani ba (su sani) ba hauka ga sahibinsu (Annabi Sallallahu alaihi wasallama) shi bai kasance ba sai mai gargaɗi mabayyanin gargaɗi, (ai mai barazana).

185. Shin basa duban zuzzurfan mulkin sammai da k̃assai, da abinda Allah ya halitta na komai (donsu kafa dalili dasu a bisa ikon wanda yayi su da kaɗaitarsa,) kuma suyi duba a cikin cewa, Yakusanta ya zamo ajalinsu Yakusa (su mutu kafirai, saboda maganar Sayyadina Abubakar kowane mutum yana wayar gari a cikin iyalinsa al-halin mutuwa tafi kusa gareshi daga hancin takalminsa, saboda haka suyi garaje izuwa imani). To da wane zance ne bayan Alk̃ur'ani zasu bada gaskiya?

186. Wanda Allah ya ɓatar dashi ba mai shiriyarsa, zamu barsu suna ɗimuwa a cikin shisshiginsu.

(YAUSHE NE TASHIN ALK̃IYAMA?)

187. Suna tambayar ka (wato mutanen Makka) game da tashin Alk̃iyama yaushe ne matabbarta? (Wato majefar angarta) [1] Cene (dasu) "Sanin ta dai yana =

1) Wato birkin Firgin ruwa.

ربع

۞ قُل لَّآ أَمْلِكُ لِنَفْسِى نَفْعًا وَلَا ضَرًّا إِلَّا مَا شَآءَ ٱللَّهُ
وَلَوْ كُنتُ أَعْلَمُ ٱلْغَيْبَ لَٱسْتَكْثَرْتُ مِنَ ٱلْخَيْرِ وَمَا مَسَّنِىَ ٱلسُّوٓءُ
إِنْ أَنَا۠ إِلَّا نَذِيرٌ وَبَشِيرٌ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿188﴾ هُوَ ٱلَّذِى خَلَقَكُم
مِّن نَّفْسٍ وَٰحِدَةٍ وَجَعَلَ مِنْهَا زَوْجَهَا لِيَسْكُنَ إِلَيْهَا فَلَمَّا
تَغَشَّىٰهَا حَمَلَتْ حَمْلًا خَفِيفًا فَمَرَّتْ بِهِۦ فَلَمَّآ أَثْقَلَت دَّعَوَا ٱللَّهَ
رَبَّهُمَا لَئِنْ ءَاتَيْتَنَا صَٰلِحًا لَّنَكُونَنَّ مِنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ﴿189﴾
فَلَمَّآ ءَاتَىٰهُمَا صَٰلِحًا جَعَلَا لَهُۥ شِرْكًا فِيمَآ ءَاتَىٰهُمَا فَتَعَٰلَى ٱللَّهُ
عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿190﴾ أَيُشْرِكُونَ مَا لَا يَخْلُقُ شَيْـًٔا وَهُمْ يُخْلَقُونَ ﴿191﴾
وَلَا يَسْتَطِيعُونَ لَهُمْ نَصْرًا وَلَآ أَنفُسَهُمْ يَنصُرُونَ ﴿192﴾
وَإِن تَدْعُوهُمْ إِلَى ٱلْهُدَىٰ لَا يَتَّبِعُوكُمْ سَوَآءٌ عَلَيْكُمْ أَدَعَوْتُمُوهُمْ
أَمْ أَنتُمْ صَٰمِتُونَ ﴿193﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ
عِبَادٌ أَمْثَالُكُمْ فَٱدْعُوهُمْ فَلْيَسْتَجِيبُوا۟ لَكُمْ إِن كُنتُمْ
صَٰدِقِينَ ﴿194﴾ أَلَهُمْ أَرْجُلٌ يَمْشُونَ بِهَآ أَمْ لَهُمْ أَيْدٍ يَبْطِشُونَ بِهَآ
أَمْ لَهُمْ أَعْيُنٌ يُبْصِرُونَ بِهَآ أَمْ لَهُمْ ءَاذَانٌ يَسْمَعُونَ بِهَا
قُلِ ٱدْعُوا۟ شُرَكَآءَكُمْ ثُمَّ كِيدُونِ فَلَا تُنظِرُونِ ﴿195﴾

= wajen Ubangijina shi Kaɗai. Ba mai bayyanata a cikin Lokacinta sai Allah. Tayi nauyi cikin sammai da ƙassai, baza tazo muku ba sai baraɓe, (wato bazato ba tsammani). "Suna tambayar ka gareta, kai kace kai mai nacin yawan tambayarta tane, "Ita dai saninta yana wajen Ubangiji shi kaɗai, amma yawaicin mutane basu san haka ba"

(MANZO MUTUMNE DA BAI MALLAKI KOMAI BA SAI GARGADI DA ALBISHIR)

188. Cene in ban mallaki amfani ko cuta ga kaina ba, sai abinda Allah yaga dama. Dana kasance na san gaibu dana yawaita alheri, da abinda bana so bai same ni ba, (na talauci da waninsa). Ni ban zamo ba illa mai barazana da wuta (ga kafirai) mai albishir da Aljanna ga mutane masu bada gaskiya. "

SHIRKA'BOYAY YA"

189. Shine wanda ya halicce ku daga kai guda daya Adamu, ya halicci mata tasa daga gareshi, (Hauwa'u) donya nutsu izuwa gareta. To, yayin daya tara da ita, saitayi ciki, ciki sassauka (shine ɗugo na maniyyi). Ta wuce dashi, (takaita kawo dashi.) Yayin da tayi nauyi (da girman ɗa a cikinta sukaji tsoron kada ya zama dabba,) sai suka roƙi Allah Ubangijinsu, Wallahi in ka bamu ɗa salihi, Lalle zamu kasance cikin masu godiya (gareka).

190. To, yayin daya basu ɗa salihi, sai suka sanya shariki a cikin abinda ya basu, (saboda sun ambace shi Abdulharisi maimakon su ce Abdullahi). Ubangiji ya girma ga buran abinda suke shirkantawa (dashi, su mutanen Makka).

191. Donme suke shirkantawa dashi a cikin bauta abinda baya halittar kome, sune ake halitta?

192. Basu da ikon taimako ga masu bauta musu, bakuma zasu iya taimakon kawukansu ba.

193. In ka kirawo waɗannan gumaka izuwa shiriya bazasu bi ku ba. Duk ɗaya ne a gare ku, kun kira su izuwa gareshi, koku masuyin shiru ne ga buran kiransu.

194. Waɗanda kuke bautawa ba Allah ba, bayi ne tamkar ku. To, ku roƙe su su amsa muku roƙon in kun zamo magaskata (a kan cewa su iyayen giji ne).

(HAƘIƘAR GUMAKA DA DODANNI)

195. Shin suna da ƙafufuwa ne dasuke tafiya dasu, ko kuwa suna da hannaye ne dasuke riƙo dasu, ko suna da idanuwa ne dasuke dubada ita, ko suna da kunnuwa ne dasuke ji dasu? A'a! (Basu da ɗaya daga cikin waɗannan, kune kuke dasu. ƙaƙa zaku bauta musu alhali ku kunfi su cikakken hali). Cene (dasu Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama,) "Ku kirawo gumakan naku (izuwa halakar da ni,) Sannan kuyi min shiri, kadaku, saurara min, (ni ban kula daku ,ba).

إِنَّ وَلِـِّۧىَ ٱللَّهُ ٱلَّذِى نَزَّلَ ٱلْكِتَٰبَ وَهُوَ يَتَوَلَّى ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿196﴾
وَٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِهِۦ لَا يَسْتَطِيعُونَ نَصْرَكُمْ وَلَآ أَنفُسَهُمْ
يَنصُرُونَ ﴿197﴾ وَإِن تَدْعُوهُمْ إِلَى ٱلْهُدَىٰ لَا يَسْمَعُوا۟ وَتَرَىٰهُمْ
يَنظُرُونَ إِلَيْكَ وَهُمْ لَا يُبْصِرُونَ ﴿198﴾ * خُذِ ٱلْعَفْوَ وَأْمُرْ بِٱلْعُرْفِ
وَأَعْرِضْ عَنِ ٱلْجَٰهِلِينَ ﴿199﴾ وَإِمَّا يَنزَغَنَّكَ مِنَ ٱلشَّيْطَٰنِ نَزْغٌ
فَٱسْتَعِذْ بِٱللَّهِ إِنَّهُۥ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿200﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوْا۟
إِذَا مَسَّهُمْ طَٰٓئِفٌ مِّنَ ٱلشَّيْطَٰنِ تَذَكَّرُوا۟ فَإِذَا هُم
مُّبْصِرُونَ ﴿201﴾ وَإِخْوَٰنُهُمْ يَمُدُّونَهُمْ فِى ٱلْغَىِّ ثُمَّ
لَا يُقْصِرُونَ ﴿202﴾ وَإِذَا لَمْ تَأْتِهِم بِـَٔايَةٍ قَالُوا۟ لَوْلَا ٱجْتَبَيْتَهَا
قُلْ إِنَّمَآ أَتَّبِعُ مَا يُوحَىٰٓ إِلَىَّ مِن رَّبِّى هَٰذَا بَصَآئِرُ مِن رَّبِّكُمْ
وَهُدًى وَرَحْمَةٌ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿203﴾ وَإِذَا قُرِئَ ٱلْقُرْءَانُ
فَٱسْتَمِعُوا۟ لَهُۥ وَأَنصِتُوا۟ لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ ﴿204﴾ وَٱذْكُر رَّبَّكَ
فِى نَفْسِكَ تَضَرُّعًا وَخِيفَةً وَدُونَ ٱلْجَهْرِ مِنَ ٱلْقَوْلِ بِٱلْغُدُوِّ
وَٱلْـَٔاصَالِ وَلَا تَكُن مِّنَ ٱلْغَٰفِلِينَ ﴿205﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ عِندَ رَبِّكَ
لَا يَسْتَكْبِرُونَ عَنْ عِبَادَتِهِۦ وَيُسَبِّحُونَهُۥ وَلَهُۥ يَسْجُدُونَ ۩ ﴿206﴾

ثمن

سجدة

196. "Hak̃ik̃a Allah ne waliyyina wanda ya saukar da Alk̃ur'ani, shine mai jiɓintar salihai.
197. "Wađanda kuke bautawa bashi ba, basu da ikon taimakon ku, basu da ikon taimokon kansu. To, yaya zan kula dasu.
198. In ka kirawo wađannan gumaka izuwa shiriya baza suji ba. Kana ganin su wađannan gumaka (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama) suna duba izuwa gareka, (sun fuskance ka kamar mai duba,) alhali su basa ganinka.

(WANI ABU DAGA TA'DODIN ALḰUR'ANI NA DAGA MU'AMULA DA MUTANE DA SHAIĐAN)

199. Yi rik̃o da rangwame,. kayi umarni da abin sani a shari'a, ka bujure ga buranjahilai.
200. Idan wani mai tunzurawa na shaiđan ya tunzura ka ga buran abinda aka umarce ka dashi,) to, nemi tsari da Allah, (Ya ije shi ga buranka). Hak̃ik̃a shi Ubangiji mai ji ne masani ne.
201. Hak̃ik̃a wađanda sukaji tsoron Allah. idan wani abu ya samesu daga shaiđan sai sukan tuna (azabar Ubangiji da sakamakonsa,) to, sai gasu suna masu ganin (gaskiya).
202. "Yan uwan shaiđanun nan na daga shaiđanun kafirai suna taimakonsu a cikin halaka kuma basa takaitawa.

(ALḰUR'ANI DAGA ALLAH YAKE)

203. Idan baka zowa mutanen Makka bada mu'ujiza (daga abinda suka shato ba,) saisu ce; "Donme baka k̃age ta ba? Cene (dasu) "Ni ina bin abinda aka aiko daga Ubangijina izuwa garenine kawai.Wannan alk̃ur'ani hujjojine daga Ubangijinku, rahama ce da jink̃ai ga mutane masu bada gaskiya".

(WANI ABU DAGA LADABIN SAURARON ALḰUR'ANI DA ZIKIRI)

204. Idan ana karanta Alk̃ur'ani, ku saurare shi kuyi shiru (ga buran kowace magana,) don a jikan ku.
205. Ka ambaci Ubangijinka a cikin zuciyarka don k̃ank̃an da kai, da tsoron Ubangiji, kuma burbushin asirtawa, koma - bayan bayyanawa, (wato tsaka tsaki) a safiya dayammaci. Kadaka zamo daga cikin marabkana (ga ambaton Allah).

Sajada

206. Haik̃ik̃a wađannan dasuke gurin Ubangijinka na Mala'iku, basa girman kai ga buran ibada tasa, suna tsarkake shi (ga buran abinda bai kamace shi ba). Kuma gareshi shi kađai suke yinsujada; (kuma ku zama kamarsu).

8 سُورَةُ الْأَنفَالِ مَدَنِيَّةٌ

وَهِيَ سِتٌّ وَسَبْعُونَ ءَايَةً 76

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ الْأَنفَالِ قُلِ الْأَنفَالُ لِلَّهِ وَالرَّسُولِ فَاتَّقُوا اللَّهَ
وَأَصْلِحُوا ذَاتَ بَيْنِكُمْ وَأَطِيعُوا اللَّهَ وَرَسُولَهُ إِن كُنتُم
مُّؤْمِنِينَ (1) إِنَّمَا الْمُؤْمِنُونَ الَّذِينَ إِذَا ذُكِرَ اللَّهُ وَجِلَتْ قُلُوبُهُمْ
وَإِذَا تُلِيَتْ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُهُ زَادَتْهُمْ إِيمَٰنًا وَعَلَىٰ رَبِّهِمْ يَتَوَكَّلُونَ (2)
الَّذِينَ يُقِيمُونَ الصَّلَوٰةَ وَمِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ يُنفِقُونَ (3) أُوْلَٰٓئِكَ
هُمُ الْمُؤْمِنُونَ حَقًّا لَّهُمْ دَرَجَٰتٌ عِندَ رَبِّهِمْ وَمَغْفِرَةٌ وَرِزْقٌ
كَرِيمٌ (4) * كَمَا أَخْرَجَكَ رَبُّكَ مِنۢ بَيْتِكَ بِالْحَقِّ وَإِنَّ فَرِيقًا مِّنَ ربع
الْمُؤْمِنِينَ لَكَٰرِهُونَ (5) يُجَٰدِلُونَكَ فِي الْحَقِّ بَعْدَ مَا تَبَيَّنَ كَأَنَّمَا
يُسَاقُونَ إِلَى الْمَوْتِ وَهُمْ يَنظُرُونَ (6) وَإِذْ يَعِدُكُمُ اللَّهُ إِحْدَى
الطَّآئِفَتَيْنِ أَنَّهَا لَكُمْ وَتَوَدُّونَ أَنَّ غَيْرَ ذَاتِ الشَّوْكَةِ تَكُونُ لَكُمْ وَيُرِيدُ
اللَّهُ أَن يُحِقَّ الْحَقَّ بِكَلِمَٰتِهِ وَيَقْطَعَ دَابِرَ الْكَٰفِرِينَ (7)
لِيُحِقَّ الْحَقَّ وَيُبْطِلَ الْبَٰطِلَ وَلَوْ كَرِهَ الْمُجْرِمُونَ (8)

Suratul Anfali

A Madina Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Saba'in Dashida (76)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabadaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe

(GANIMA)

'Wannan sura ta ƙunshi ƙissoshin da suka ƙebanta ga Manzon Allah, ballantana Lokacin yaƙe - yaƙe da Hijira,wacce take gabanta. Kuma ta ƙunshi ƙissoshin Annabawa ne gabaɗaya tsiran Allah da amincinsa su tabbata a garesu"

(GANIMA)

1. Suna tambayar ka (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama a kan ganimomi ta wace ce? Cene (dasu) "Ganimomi na Allah ne da manzonsa. (suna ajiye ta a inda suka ga dama, sai Annabi Sallallahu alaihi wasallama ya rabata tsakaninsu daidai wadaida, kamar yadda Hakimu ya ruwaito a cikin Mustadaraku) Ku tsoraci Allah ku gyara haluluwan tsakanin ku, ayi soyayya a daina jayayya, kubi Allah kubi Ma'aikinsa in kun kasance muminai, (muminai na gaskiya).
2. Muminai (masu cikakken imani) sune waɗanda idan aka ambaci Allah sai zukatansu ta ji tsoro, idan an karanta ayoyinsa a garesu saita ƙara musu imani a bisa Ubangijinsu kadai suke dogara.
3. Waɗanda suke tsayar da sallah (suke bada hakkokin sallah na zahiri dana badini,) suke ciyar-wa daga abinda muka azurta musu (a cikin da'ar Allah).
4. Waɗancananka su kaɗai ne muminai na gaskiya, darajoji na garesu nan ga Ubangijinsu, (sune maƙamomi keɓantattu a cikin Aljanna,) da gafara da arziki maigirma.

(ABINDA YA TABBATA GA ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA ZAMANIN FITARSA YAKIN BADAR BABBA)

"Wannan hali a cikin ƙinsu gareta kamar fitar dakai ne a cikin halin ƙinsu, alhali ya kasance mafi alheri garesu, to haka nan wannan".

5. Yadda Ubangijinka yafitar dakai daga ɗakinka da gaskiya, alhali waɗansu jama'a na mumi-nai Lalle masu ƙi ne (ga wannan fita).
6. Suna jayayya dakai a cikin gaskiya (wato yaƙi) bayan ya bayyana garesu, kai kace ana kora sune izuwa mutuwa, alhali su suna duba (izuwa gareshi da idanuwansu).
7. Ka ambata zamanin da Ubangiji yake yi muku alƙawarin jama'a guda biyu, (ayarin fatauci ko ƙungiyar yaƙi,) cewa ita taku ce, alhali ku kuna son cewa wata ma'abuciyar kaya ta kasance gareku. (saboda ƙarancin adadin ƙungiyar da tanajinta,) Allah yana nufin ya tabbatar da gaskiya, da kalmominsa, (da rinjayen Musulunci,) ya yanke asalin kafirai, (saboda haka ya umarce ku dayaƙin kungiyar yaƙi).
8. Donya tabbatar da gaskiyaya ɓata ƙarya (wato kafirci,) ko da mushirikai sun ƙi wannan.

(WANI ABU DAGA SABABAN NASARA A YAƘIN BADAR)

إِذْ تَسْتَغِيثُونَ رَبَّكُمْ فَاسْتَجَابَ لَكُمْ أَنِّي مُمِدُّكُم
بِأَلْفٍ مِّنَ الْمَلَائِكَةِ مُرْدِفِينَ ﴿٩﴾ وَمَا جَعَلَهُ اللَّهُ إِلَّا بُشْرَىٰ
وَلِتَطْمَئِنَّ بِهِ قُلُوبُكُمْ وَمَا النَّصْرُ إِلَّا مِنْ عِندِ اللَّهِ إِنَّ اللَّهَ
عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿١٠﴾ إِذْ يُغَشِّيكُمُ النُّعَاسَ أَمَنَةً مِّنْهُ وَيُنَزِّلُ عَلَيْكُم
مِّنَ السَّمَاءِ مَاءً لِّيُطَهِّرَكُم بِهِ وَيُذْهِبَ عَنكُمْ رِجْزَ الشَّيْطَانِ
وَلِيَرْبِطَ عَلَىٰ قُلُوبِكُمْ وَيُثَبِّتَ بِهِ الْأَقْدَامَ ﴿١١﴾ * إِذْ يُوحِي رَبُّكَ ثمن
إِلَى الْمَلَائِكَةِ أَنِّي مَعَكُمْ فَثَبِّتُوا الَّذِينَ آمَنُوا سَأُلْقِي
فِي قُلُوبِ الَّذِينَ كَفَرُوا الرُّعْبَ فَاضْرِبُوا فَوْقَ الْأَعْنَاقِ
وَاضْرِبُوا مِنْهُمْ كُلَّ بَنَانٍ ﴿١٢﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ شَاقُّوا اللَّهَ وَرَسُولَهُ
وَمَن يُشَاقِقِ اللَّهَ وَرَسُولَهُ فَإِنَّ اللَّهَ شَدِيدُ الْعِقَابِ ﴿١٣﴾
ذَٰلِكُمْ فَذُوقُوهُ وَأَنَّ لِلْكَافِرِينَ عَذَابَ النَّارِ ﴿١٤﴾
يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا إِذَا لَقِيتُمُ الَّذِينَ كَفَرُوا زَحْفًا
فَلَا تُوَلُّوهُمُ الْأَدْبَارَ ﴿١٥﴾ وَمَن يُوَلِّهِمْ يَوْمَئِذٍ دُبُرَهُ
إِلَّا مُتَحَرِّفًا لِّقِتَالٍ أَوْ مُتَحَيِّزًا إِلَىٰ فِئَةٍ فَقَدْ بَاءَ
بِغَضَبٍ مِّنَ اللَّهِ وَمَأْوَاهُ جَهَنَّمُ وَبِئْسَ الْمَصِيرُ ﴿١٦﴾

9. Zamanin da kuke neman Ubangijinku ya amsa muku, cewa ni mai taimakonkune da dubu na Mala'iku masu bibiyan juna.
10. Allah bai sanya wannan taimako ba sai don albishir gareku. Kuma don zukatanku su nutsu dashi, Taimako bai kasance ba sai daga Allah. Haƙiƙa Ubangiji mabuwayi ne gwani.
11. Ka ambata zamanin da yake saka muku gyangyaɗi don amintarwa daga gareshi, (daga abinda ya tabbata a gareku na tsoro,) yake sassaukar da ruwa daga sama gareku donya tsarkake ku dashi (daga karrai da janaba,) yana tafiyar da wasuwasin shaiɗan ga buranku. Kuma donya ɗaure zukatanku (da yaƙini da hakuri,) yana tabbatar da digadiganku dashi (wannan ruwa don kadaku, afe a cikin rairayi).
12. Yayin da Ubangijinka yake aikowa izuwa Mala'iku (waɗandaya taimaki Musulmi dasu,) cewa Ni ina taredaku ,(da taimako da agaji,) ku tabbatar da waɗanda suka bada gaskiya (da taimako da albishir). Da sannu zan jefa razani a cikin zukatan waɗanda suka kafirta. Ku doki birbishin wuyayu, ku doke dukkan gyaffa nasu na hannaye da ƙafafuwa (sai mutum yanufi sare wuyan kafiri, sai yaga wuyan a ƙasa tun kafin kansakalinsa bai sadu izuwa wuyan kafirin ba, anan ne Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama ya jefe su da damƙe ɗaya na tsakwankwani ta cika idanuwan dukkan mushirikan da suka halarci wannan yaƙi sai suka risɓa).
13. Wancananka (azabadaya sauka garesu) saboda haƙiƙa sun saɓawa Allah da ma'aikinsa ne, wanda ya saɓawa Allah da ma'aikinsa haƙiƙa Ubangiji mai tsananin azabane gareshi.
14. Wancananka azabaku ɗanɗane shi (a duniya). Haƙiƙa azabar wuta ta tabbata ga kafirai (a Lahira).

(DABARE - DABARE NA YAKI GA MUMINAI)

15. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya, idan kun gamu da kafirai (sun yi dafifi,) to, kadaku ,basu baya.
16. Wanda ya juya musu baya a wannan rana, in dai ba mai waskacewa don dabarar yaƙi ba, ko mai tattara izuwa wata ƙungiya ta rundunar yaƙin wasu Musulmi, to haƙiƙa yakoma da fushi daga Allah, Jahannama ce makoma tasa tir da makoma ita! (To wannan fa idan kafiran basu zamo ninke - ninken Musulmi ba ne).

فَلَمْ تَقْتُلُوهُمْ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ قَتَلَهُمْ ۚ وَمَا رَمَيْتَ إِذْ رَمَيْتَ
وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ رَمَىٰ ۚ وَلِيُبْلِيَ ٱلْمُؤْمِنِينَ مِنْهُ بَلَآءً حَسَنًا ۚ إِنَّ ٱللَّهَ
سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿17﴾ ذَٰلِكُمْ وَأَنَّ ٱللَّهَ مُوهِنُ كَيْدِ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿18﴾
إِن تَسْتَفْتِحُواْ فَقَدْ جَآءَكُمُ ٱلْفَتْحُ ۖ وَإِن تَنتَهُواْ فَهُوَ خَيْرٌ
لَّكُمْ ۖ وَإِن تَعُودُواْ نَعُدْ وَلَن تُغْنِيَ عَنكُمْ فِئَتُكُمْ شَيْـًٔا
وَلَوْ كَثُرَتْ وَأَنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿19﴾ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَا تَوَلَّوْاْ عَنْهُ وَأَنتُمْ
تَسْمَعُونَ ﴿20﴾ وَلَا تَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ قَالُواْ سَمِعْنَا وَهُمْ لَا يَسْمَعُونَ ﴿21﴾
۞ إِنَّ شَرَّ ٱلدَّوَآبِّ عِندَ ٱللَّهِ ٱلصُّمُّ ٱلْبُكْمُ ٱلَّذِينَ
لَا يَعْقِلُونَ ﴿22﴾ وَلَوْ عَلِمَ ٱللَّهُ فِيهِمْ خَيْرًا لَّأَسْمَعَهُمْ ۖ
وَلَوْ أَسْمَعَهُمْ لَتَوَلَّواْ وَّهُم مُّعْرِضُونَ ﴿23﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ ٱسْتَجِيبُواْ لِلَّهِ وَلِلرَّسُولِ إِذَا دَعَاكُمْ لِمَا يُحْيِيكُمْ ۖ
وَٱعْلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ يَحُولُ بَيْنَ ٱلْمَرْءِ وَقَلْبِهِۦ وَأَنَّهُۥٓ
إِلَيْهِ تُحْشَرُونَ ﴿24﴾ وَٱتَّقُواْ فِتْنَةً لَّا تُصِيبَنَّ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ
مِنكُمْ خَآصَّةً ۖ وَٱعْلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ﴿25﴾

ربع

17. Baku kashe su (a Badar da ƙarfin ku ba). Kai dai Allah ne ya kashe su daya taimake ku, kuma bakaine kajefi idanuwan mutanen nan ba (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama,) zamanin da kayi jifa da tsak-wankwani, (domin cikin tafi na tsakuwa bazai cika idanuwan mayaka da yawa ba, da jifan ɗan Adam,) kai dai Allah ne yayi jifan, (da sada wancananka izuwa garesu. yayi wannan donya rinjayi kafirai,) domin kuma ya kyautata wa muminai kyautatawa kyakkyawa daga gareshi (shine ganima). Ubangiji mai ji ne da komai masani da komai.

18. Wancananku (kyautatawa gaskiya ne,) kuma haƙiƙa Ubangiji mai raunana kaidin kafirai ne.

19. In kun nemi hukunci (Yaku waɗannan kafirai, Lokacin da Abu - Jahil yake cewa: Ubangiji kowannenmu ya kasance mafi yankewa ga zumunta, yazo mana da abinda bamu sani ba, halakar dashi a yau yau ɗinnan,) to, haƙiƙa hukunci yazo muku (da halakar wanda yake shine haka din, Abu - Jahil da wanda aka kashe tare dashi, ba Annabi da muminai ba). Idan kun hanu (ga buran kafirci dayaƙi,) to, shi yafi alheri gareku, in kun komo (ga yaƙin Annabi Sallallahu alaihi wasallama,) ma komo (da taimakonsa a kanku,) rundunar ku baza tayi muku amfanin kome ba, kome yawanta. Haƙiƙa Ubangiji yana tareda muminai.

(TSORATARWA DAGA SABA WA ADDINI)

20. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! Kubi Allah da ma'aikinsa, kadaku ,bada bayaga buransa (da saɓa umarninsa,) alhali kuna jin (gargaɗin alƙur'ani).

21. Kadaku ,kasance kamar waɗanda Sukace, "Mun ji, alhali su ba jin fahimta sukayi ba, (munafukai da mushurikai Kenan.)

22. Haƙiƙa mafi sharrin dabbobi nan ga Allah, kurame (ga buran jin gaskiya,) bebaye (ga buran faɗar gaskiya,) waɗanda basa hankaltar (komai).

23. Da Allah yasan alheri cikinsu dayaji dasu (jin fahimta). Da kuma yaji dasu ɗin (taƙadiran alhali yasan babu alheri cikinsu) dasun juya (ga buransa alhali) su suna masu bujirewa (ga buran karɓarsa).

(AMSAWA GA MAKIRAYIN ALƘUR'ANI)

24. Ya waɗanda suka bada gaskiya! Ku amsawa Allah da Manzonsa (da ɗa'a) idan ya kira ku izuwa abinda yake raYaku, (cikin Lamarin addini, domin shine sababin rayuwa ta tutur). Ku sani haƙiƙa Allah yana tsarewa tsakanin mutum da zuciyarsa, (bashi da ikon ya bada gaskiyako ya kafirta saida ikon Allah,) kuma haƙiƙa Ubangiji izuwa gareshi ake tara ku (yayi muku sakamako da ayyukanku).

25. Kuji tsoron fitina in ta same ku, bazata sami waɗanda sukayi zalunci daga gareku su kaɗai ba, (a'a, gama ku za tayi. To, tsoron ta kuwa yana samuwa da musun abinda yake kawo ta na aikin munkari.) Ku sani Allah mai tsananin uƙubane (ga wanda ya saɓe shi).

وَاذْكُرُوٓاْ إِذْ أَنتُمْ قَلِيلٞ مُّسْتَضْعَفُونَ فِي الْأَرْضِ
تَخَافُونَ أَن يَتَخَطَّفَكُمُ النَّاسُ فَـَٔاوَىٰكُمْ وَأَيَّدَكُم بِنَصْرِهِۦ
وَرَزَقَكُم مِّنَ الطَّيِّبَٰتِ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿26﴾ يَٰٓأَيُّهَا
الَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَخُونُواْ اللَّهَ وَالرَّسُولَ وَتَخُونُوٓاْ أَمَٰنَٰتِكُمْ
وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿27﴾ وَاعْلَمُوٓاْ أَنَّمَآ أَمْوَٰلُكُمْ وَأَوْلَٰدُكُمْ
فِتْنَةٞ وَأَنَّ اللَّهَ عِندَهُۥٓ أَجْرٌ عَظِيمٞ ﴿28﴾ يَٰٓأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ
إِن تَتَّقُواْ اللَّهَ يَجْعَل لَّكُمْ فُرْقَانٗا وَيُكَفِّرْ عَنكُمْ سَيِّـَٔاتِكُمْ
وَيَغْفِرْ لَكُمْ وَاللَّهُ ذُو الْفَضْلِ الْعَظِيمِ ﴿29﴾ وَإِذْ يَمْكُرُ
بِكَ الَّذِينَ كَفَرُواْ لِيُثْبِتُوكَ أَوْ يَقْتُلُوكَ أَوْ يُخْرِجُوكَ وَيَمْكُرُونَ
وَيَمْكُرُ اللَّهُ وَاللَّهُ خَيْرُ الْمَٰكِرِينَ ﴿30﴾ وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُنَا
قَالُواْ قَدْ سَمِعْنَا لَوْ نَشَآءُ لَقُلْنَا مِثْلَ هَٰذَآ إِنْ هَٰذَآ إِلَّآ أَسَٰطِيرُ
الْأَوَّلِينَ ﴿31﴾ ۞ وَإِذْ قَالُواْ اللَّهُمَّ إِن كَانَ هَٰذَا هُوَ الْحَقَّ مِنْ ثمن
عِندِكَ فَأَمْطِرْ عَلَيْنَا حِجَارَةٗ مِّنَ السَّمَآءِ أَوِ ائْتِنَا
بِعَذَابٍ أَلِيمٖ ﴿32﴾ وَمَا كَانَ اللَّهُ لِيُعَذِّبَهُمْ وَأَنتَ فِيهِمْ
وَمَا كَانَ اللَّهُ مُعَذِّبَهُمْ وَهُمْ يَسْتَغْفِرُونَ ﴿33﴾

26. Ku ambata Lokacin da kuke kaɗan, raunana a cikin ƙasar Makka, kuna jin tsoron mutane su fyauce ku, ya tattara ku (izuwa Madina,) ya ƙarfafe kuda nasarar sa aranar badar da -mala'iku, ya azurta kuda ganimomin yaƙi don ku gode wa (ni'imominsa).

(HA'INCI YANA DAGA SIFFAR MUNAFIKAI)

"Yayin da Abu - Lubabata Marwanu dan Abdulmunziri, Annabi Sallallahu alaihi wasallama ya aike shi izuwa Bani - ƙuraizata, donsu sauka a kan hukuncinsa, suka nemi shawararsa saiya basu haske da nuna musu cewa yanka ne, domin iyalinsa da dukiyarsa tana wurinsu, sai Ubangiji yace:"

27. Yaku waɗanda suka bada gaskiya, kadaku ,ha'inci Allah da manzansa, kadaku, ha'inci amanonin ku (na addini da waninsa, alhali ku kuna masana da haramcin haka.

28. Kuma ku sani ba wani abu ne dukiyoyinkuda "ya" yayenku ba illa fitina ce kawai a gareku, (mai hana ku al'amarin Lahira,) Ubangiji Lada maigirma ya tabbata a gareshi. kadaku ,tse radda lada sabo da dukiyoyi da 'ya'ya ye.

(TSORON ALLAH DA AMFANINSA)

29. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! In kun ji tsoron Allah zai sanya muku haske dazai dinga rabe muku tsakanin ƙarya da gaskiya, zai kankare muku miyagun ayyukanku, zai gafarta muku zunubanku, Ubangiji ma'abucin falala! ne maigirma.

(ADAWARSU DA MANZON ALLAH DA ADDININSU)

30. Ka ambata (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama,) zamanin da kafirai suke maƙirci da kai, (alhali sun yi taro saboda shawara a cikin sha'aninka a (gidan shawara,) donsu ɗaure ka, ko su kashe ka dukkansu kisan mutum ɗaya, ko su fitar dakai daga Makka, suna shirya maka makirci, Allah yana shirya sakamakon makircin nan a garesu. Allah shine mafi iya sakamakon makirci.

31. Idan ana karantawar ayoyinmu, (ƙur'ani) a garesu sukan ce, "Mun ji, da munga dama da mun faɗi irin wannan, (inji Nadhru ɗan Harisu shine mai zuwa (Hirata) gari ne a kusa da Kufa yana fatauci saiya sayo Littattafan bebayin can ya kawo wa mutanen Makka). Wannan Alƙur'ani bai kasance ba sai ƙaryace - ƙaryacen mutanen farko".

(WANI ABU NA DAGA WAUTAR LARABAWA DA JAHILIYYARSU)

32. A yayin dayace; "Ya Ubangiji in wannan alƙur'ani ya kasance shine gaskiya daga gareka, to, sako da ruwan duwarwatsu a kanmu, ko kazo mana da azaba mai raɗaɗi". (Ya faɗi wannan ne don izgili kuma da wahimtarwa wai cewa yana a kan basira da yaƙinine rashin gaskiyar Alƙur'ani).

33. (Sai Ubangiji yace,) "Allah bai kasance zaiyi musu azaba ba (saboda wannan katobara) alhali kai kana cikinsu (domin azaba in ta sauka gamawa take. Ba a taɓayi wa wata al'umma azaba ba sai bayan fitar Annabintada muminai daga cikinta,) Allah bazaiyi musu azaba ba alhali su suna neman gafara. (saboda raunanan muminan da suka ragu a Makka bayan fitar manzon Allah)"."Bayan fitar Manzon Allah 'Sallallahu alaihi wasallama' da raunanan muminai daga Makka, sai Ubangiji ya saukar:"

وَمَا لَهُمْ أَلَّا يُعَذِّبَهُمُ اللَّهُ وَهُمْ يَصُدُّونَ عَنِ
الْمَسْجِدِ الْحَرَامِ وَمَا كَانُوا أَوْلِيَاءَهُ ۚ إِنْ أَوْلِيَاؤُهُ
إِلَّا الْمُتَّقُونَ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿34﴾ وَمَا كَانَ صَلَاتُهُمْ
عِندَ الْبَيْتِ إِلَّا مُكَاءً وَتَصْدِيَةً ۚ فَذُوقُوا الْعَذَابَ بِمَا
كُنتُمْ تَكْفُرُونَ ﴿35﴾ إِنَّ الَّذِينَ كَفَرُوا يُنفِقُونَ أَمْوَالَهُمْ
لِيَصُدُّوا عَن سَبِيلِ اللَّهِ ۚ فَسَيُنفِقُونَهَا ثُمَّ تَكُونُ
عَلَيْهِمْ حَسْرَةً ثُمَّ يُغْلَبُونَ ۗ وَالَّذِينَ كَفَرُوا
إِلَىٰ جَهَنَّمَ يُحْشَرُونَ ﴿36﴾ لِيَمِيزَ اللَّهُ الْخَبِيثَ مِنَ
الطَّيِّبِ وَيَجْعَلَ الْخَبِيثَ بَعْضَهُ عَلَىٰ بَعْضٍ فَيَرْكُمَهُ جَمِيعًا
فَيَجْعَلَهُ فِي جَهَنَّمَ ۚ أُولَٰئِكَ هُمُ الْخَاسِرُونَ ﴿37﴾ قُل لِّلَّذِينَ
كَفَرُوا إِن يَنتَهُوا يُغْفَرْ لَهُم مَّا قَدْ سَلَفَ وَإِن يَعُودُوا
فَقَدْ مَضَتْ سُنَّتُ الْأَوَّلِينَ ﴿38﴾ وَقَاتِلُوهُمْ حَتَّىٰ لَا تَكُونَ
فِتْنَةٌ وَيَكُونَ الدِّينُ كُلُّهُ لِلَّهِ ۚ فَإِنِ انتَهَوْا
فَإِنَّ اللَّهَ بِمَا يَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿39﴾ وَإِن تَوَلَّوْا فَاعْلَمُوا
أَنَّ اللَّهَ مَوْلَاكُمْ ۚ نِعْمَ الْمَوْلَىٰ وَنِعْمَ النَّصِيرُ ﴿40﴾

34. Menene ke garesu da Allah bazaiyi musu azaba (da kansakali) ba, alhali su suna hana (Annabi Sallallahu alaihi wasallama) ga masallaci mai alfarma (ga buran ɗawafi da ibada a ciki,) su basu kasance masoya Allah ba. Ba waɗansune waliyyan Allah ba sai masu tsoron Allah, sai dai yawaicinsu basu san (haka ba).

35. Sallarsu nan ga Daki bata kasance ba sai feɗuwa da tafi, (su feɗuwa da tafi suke yi maimakon sallar ɗa aka umarce su da ita). To, ku ɗanɗani azaba abadan saboda zaluncinku.

(AƘIBAR CIYARWARSU DON HANA ADDININ ALLAH)

36. Waɗannan da suka kafirta suna ciyar da dukiyoyinsu (a cikin yaƙi da Annabi Sallallahu alaihi wasallama) donsu hana ga buran addinin Allah. To, da sannu zasu ciyar da ita sannan a ƙarshen al'amari ya zamo nadama a garesu, sannan a rinjaye su a duniya. Waɗanda suka kafirta a cikinsu ana tara sune izuwa Jahannama (Ranar Alƙiyama).

37. Don Allah ya nuna mugu daga tsatstsarkan mumini, yasanya mugu sashinsa a kan sashi, ya Labta su bakiɗaya, dukkansu ya ruguntsuma su a cikin Jahannama. Waɗancananka su ne taɓaɓɓu.

(WANI ABU DAGA FALALAR, UBANGIJI A KAN MUTANE)

38. Ka faɗa ga waɗanda suka kafirta (kamar Abi - Sufiyana da abokansa) in sun hanu ga buran kafirci dayaƙin Annabi Sallallahu alaihi wasallama,) a gafarta musu abinda yagabata (na ayyukansu). In sun komo (izuwa yaƙinsa,) haƙiƙa al'adarmu a cikin mutanen farko da suka wuce (hakana zamuyi musu su ma).

(WAJABCIN YAƘI AKAN MUSULMI HAR RANDA MUSULUNCI YAGAMA DUNIYA BAKIDAYA)

39. Ku yake su har kada a sami shirka a bayan ƙasa, addini dukkansa ya kasance ga Allah shi kaɗai ba a bautawa waninsa. Idan suka hanu (ga buran kafirci,) haƙiƙa Ubangiji masanine ga abinda suke aikatawa (zaiyi musu sakamako).

40. Idan sun bada baya (ga buran imani,) to, ku sani haƙiƙa Allah mai taimakonku ne, (a cikin al'amuranku). Madalla mai taimako (Ubangiji!) Madalla mai agaji (a gareku shi!).

(YADDA AKE RABA GANIMA)

حزب

۞ وَاعْلَمُوٓاْ أَنَّمَا غَنِمْتُم مِّن شَيْءٖ فَأَنَّ لِلَّهِ خُمُسَهُۥ وَلِلرَّسُولِ
وَلِذِي ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَٰمَىٰ وَٱلْمَسَٰكِينِ وَٱبْنِ ٱلسَّبِيلِ إِن كُنتُمْ
ءَامَنتُم بِٱللَّهِ وَمَآ أَنزَلْنَا عَلَىٰ عَبْدِنَا يَوْمَ ٱلْفُرْقَانِ يَوْمَ ٱلْتَقَى
ٱلْجَمْعَانِ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٖ قَدِيرٌ ﴿41﴾ إِذْ أَنتُم بِٱلْعُدْوَةِ
ٱلدُّنْيَا وَهُم بِٱلْعُدْوَةِ ٱلْقُصْوَىٰ وَٱلرَّكْبُ أَسْفَلَ مِنكُمْ
وَلَوْ تَوَاعَدتُّمْ لَٱخْتَلَفْتُمْ فِي ٱلْمِيعَٰدِ وَلَٰكِن لِّيَقْضِيَ ٱللَّهُ
أَمْرٗا كَانَ مَفْعُولٗا ﴿42﴾ لِّيَهْلِكَ مَنْ هَلَكَ عَنۢ بَيِّنَةٖ
وَيَحْيَىٰ مَنْ حَيَّ عَنۢ بَيِّنَةٖ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَسَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿43﴾
إِذْ يُرِيكَهُمُ ٱللَّهُ فِي مَنَامِكَ قَلِيلٗا وَلَوْ أَرَىٰكَهُمْ كَثِيرٗا
لَّفَشِلْتُمْ وَلَتَنَٰزَعْتُمْ فِي ٱلْأَمْرِ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ سَلَّمَ إِنَّهُۥ عَلِيمُۢ
بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ﴿44﴾ وَإِذْ يُرِيكُمُوهُمْ إِذِ ٱلْتَقَيْتُمْ فِيٓ أَعْيُنِكُمْ
قَلِيلٗا وَيُقَلِّلُكُمْ فِيٓ أَعْيُنِهِمْ لِيَقْضِيَ ٱللَّهُ أَمْرٗا
كَانَ مَفْعُولٗا وَإِلَى ٱللَّهِ تُرْجَعُ ٱلْأُمُورُ ﴿45﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا لَقِيتُمْ فِئَةٗ فَٱثْبُتُواْ
وَٱذْكُرُواْ ٱللَّهَ كَثِيرٗا لَّعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿46﴾

41. Ku sani cewa dai abinda kuka ribata (daga kafirai na ko Menene wato kuka ƙarbe tilas daga garesu) to, Allah (yana da humusinsa, wato ɗaya a cikin biyar 1/5 yana umarni dashi a abinda yaga dama,) kuma na Manzon Allah ne (Sallallahu alaihi wasallama) da ma'abuta dangantakarsa (na Bani - Hashim da Bani Abdul - Mudallibi,) da marayu, (wato jariran Musulmi waɗanda iyayensu suka mutu, alhali basu da komai,) da miskinai, (wato ma'abutan buƙata na daga Musulmi,) da wanda guzuri ya yanke masa cikin tafiyarsa (na daga Musulmi, ai Manzon Allah ne ya cancance shi da waɗannan nau'o'in guda hudu, bisa yadda Manzon Allah ya kasance yana rabashi, wato shine cewa kow-ane ɗaya yana da humusin humisi, wato ɗaya bisa biyar ɗinnan na Allah shi ake kasawa gida biyar kowa ya ɗauki kashi ɗaya daga ciki, cewa humusai guda hudu kuwa da suka ragu na "ya'yan ganima ne wato mayaƙa,) in kun kasance kun bada gaskiya da Allah, (to, ku san haka,) da kuma abinda aka saukar a bisa bawanmu, (Annabi Sallallahu alaihi wasallama, na mala'ikuda ayoyi,) ranar Ba-dar, mai rabewa tsakanin ƙarya da gaskiya, ranar da ƙungiya guda biyu suka hadu (Musulmai da kafirai). Ubangiji mai iko ne bisa komai.

(GORIN ALLAH BISA MUMINAI A INDAYA TAIMAKE SU BISA WANDA YAFI SU ƘARFI)

42. Zamanin da kuke gaci mafi kusanci daga Madina, gefen zaza, su suna gaci mafi nisa daga Ma-dina, ga kuma ayarin na Abu -Sufiyana a guri da yake mafi kusa daku ,daga abinda yake bin kogi. Da kun yi alƙawari (ku dasu, kuda "yan yaƙin kafirai saboda yaƙi,) da sai ku saba a cikin alƙawari. Sai dai Ubangiji (ya sa kun yi kaciɓis dasu bada alƙawari ba,) donya gudanar da al'amari abin aikatawa (a saninsa, shine taimakon Musulunci da shafe kafirci).

43. (Ya aikata wannan) don wanda ya halaka ya halaka da hujja, (shine taimakon muminai tareda rauninsu a kan rundunar kafirai tareda ƙarfinsu,) wanda ya rayu ya rayu bayan hujja. Haƙiƙa Ubangiji Lalle mai ji ne masani.

44. Ka ambata zamanin da Ubangiji yake nuna maka su cum, (wato kaɗan a cikin baccinka,) (ka ba wa sahabbanka labari sukayi farin ciki). Daya nuna maka su da yawa, da kun yi raki, da kun sassaba a cikin Lamarin (yaƙinsu). Sai dai Allah Ya kuɓutar (daku ,daga wannan raki da sassaɓawa). Haƙiƙa shi masanine da haluluwan zukatan bayi.

45. Ka ambata kuma zamanin da yake nuna muku kaɗan a ganin idanuwanku zamanin da kuka gamu dasu cum, (Yaku mumi-nai, saɓa'in ne ko ɗari, alhali su dubu ne, don ku faɗa musu) yake ƙaranta ku a idanuwansu, (donsu faɗa muku. Wannan gaban ruguntsimewar yaƙi ne, a yayin daya runguntsime sai suka ga Musulmi sun ninka su biyu,) don Ubangiji ya gudanar da al'amari abin sani a cikin saninsa, Izuwa Allah al'amura duka suke komawa.

(NASIHOHIN ALƘUR'ANI A DAGAR YAƘI)

46. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! idan kun gamu da jama'a (wacce take kafira,) to, ku dage (dayaƙinsu, kadaku, ja da baya,) ku ambaci Allah ambato maiyawa, don ku rabauta.

وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَا تَنَٰزَعُواْ فَتَفۡشَلُواْ وَتَذۡهَبَ
رِيحُكُمۡۖ وَٱصۡبِرُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ﴿47﴾ وَلَا تَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ
خَرَجُواْ مِن دِيَٰرِهِم بَطَرٗا وَرِئَآءَ ٱلنَّاسِ وَيَصُدُّونَ
عَن سَبِيلِ ٱللَّهِۚ وَٱللَّهُ بِمَا يَعۡمَلُونَ مُحِيطٞ ﴿48﴾ وَإِذۡ زَيَّنَ
لَهُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ أَعۡمَٰلَهُمۡ وَقَالَ لَا غَالِبَ لَكُمُ ٱلۡيَوۡمَ مِنَ
ٱلنَّاسِ وَإِنِّي جَارٞ لَّكُمۡۖ فَلَمَّا تَرَآءَتِ ٱلۡفِئَتَانِ نَكَصَ
عَلَىٰ عَقِبَيۡهِ وَقَالَ إِنِّي بَرِيٓءٞ مِّنكُمۡ إِنِّيٓ أَرَىٰ مَا لَا تَرَوۡنَ
إِنِّيٓ أَخَافُ ٱللَّهَۚ وَٱللَّهُ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ﴿49﴾ ۞ إِذۡ يَقُولُ ٱلۡمُنَٰفِقُونَ ثمن
وَٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٌ غَرَّ هَٰٓؤُلَآءِ دِينُهُمۡۗ وَمَن
يَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٞ ﴿50﴾ وَلَوۡ تَرَىٰٓ إِذۡ
يَتَوَفَّى ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ يَضۡرِبُونَ وُجُوهَهُمۡ
وَأَدۡبَٰرَهُمۡ وَذُوقُواْ عَذَابَ ٱلۡحَرِيقِ ﴿51﴾ ذَٰلِكَ بِمَا قَدَّمَتۡ
أَيۡدِيكُمۡ وَأَنَّ ٱللَّهَ لَيۡسَ بِظَلَّٰمٖ لِّلۡعَبِيدِ ﴿52﴾ كَدَأۡبِ
ءَالِ فِرۡعَوۡنَ وَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ
فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُ بِذُنُوبِهِمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ قَوِيّٞ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ﴿53﴾

47. Kubi Allah da manzonsa, kada kuyi jayayya (a tsakaninku,) sai kuyi raki ƙarfin daular ku ya kau. Ku daure, haƙiƙa Allah yana tareda masu dauriya (da agaji da taimako).

48. Kadaku ,zamo kamar waɗannan da suKafita daga gidaddajinsu donsu hana ayarinsu, basu komo ba bayan tsiran ta, sun fita don ƙasaita, dariyaga mutane (Lokacin dasuke cewa "Bazasu komo ba sai sun bugu da giya, sun soke raƙuma, zabiyoyi sun kada musu take, duk duniya ta ji su,) suna hana mutane ga addinin Allah. Allah mai kewayewa ne da abinda suke aikatawa, (zaiyi musu sakamako dashi).

(YADDA SHAIƊAN YAKE ZUƘEWA GA KAFIRAI YAYIN TSANANI)

49. Ambaci zamanin da shaiɗan ya Kawata musu ayyukansu, (shine ya ƙarfafa zukatansu a bisa faɗawa Musulmi, yayin da sukaji tsoron magautansa Bani -Bakarin yayin fita daga Makka saboda yakinsu,) sai shaiɗan yace (dasu) 'Ba wani daga mutane dazai rinjaye ku a yau, ni mai kiwon kune (daga Bani - kinanata". Ya kasance yazo musu a cikin surar Surakatu Dan Maliku, shugaban wannan nahiyar). Yayin da jama'a guda biyu suka hadu (Musulmai da kafirai yaga Mala'iku, da kuwa hannunsa yana cikin hannun Harisu ɗan Hishamu,) saiya girka aguje a kan dugadugansa, yace (dasu "yayin da sukace dashi, yaya zaka zuƙe ka bar mu a cikin wannan hali, "Haƙiƙa ni makubuci ne daga gareku ba ruwana daku ,haƙiƙa ni ina ganin abinda ba kwa gani (na Mala'iku). Haƙiƙa ni ina tsoron Allah (ya halakar da ni,) Allah mai tsananin uƙuba ne".

50. Yayin da munafukai suke faɗa, ga waɗanda raunin imani yake cikin zuciyarsu, cewa addinin waɗannan Musulmi shine ya ruɗe su (suka fito tareda karamcinsu su yaƙi taro mai yawa, don wahamin cewa su sa sami nasara saboda addinin. Sai Ubangiji ya faɗa a cikin amsarsu,) "Wanda ya dogara ga Allah, haƙiƙa Ubangiji mabuwayi ne gwani (cikin aikinsa).

51. Da kana duba (Ya Muhammadu Sallallahu alaika wasallama,) zamanin da Mala'iku suke karɓar rayukan waɗanda suka kafirta, suna dukan fuskokinsu, da bayayyakinsu, (da gudumai na baƙin ƙarfe, suna cewa dasu) "Ku ɗanɗani azabar wuta (da kaga al'amari maigirma)".

52. Wancananka (azabtawa) saboda abinda hannuwansu ta gabatar ne, haƙiƙa Ubangiji ba mai zalunci ne da bayi ba, (yayi musu azaba bada zunubi ba).

(ABINDA YA SAMESU SABODA AYYUKANSU)

53. (Halinsu da al'adarsu) kamar ta Fir'auna ce da mutanensa da waɗanda suke gabansu, sun kafirtada ayoyin Allah, Ubangiji saiya kama su (da uƙuba) saboda zunubansu. Haƙiƙa Ubangiji ƙaƙƙarfa ne (bisa abinda yake nufi,) mai tsananin uƙuba ne.

ذَٰلِكَ بِأَنَّ اَ۬للَّهَ لَمْ يَكُ مُغَيِّراً نِّعْمَةً اَنْعَمَهَا عَلَىٰ قَوْمٍ حَتَّىٰ
يُغَيِّرُواْ مَا بِأَنفُسِهِمْ وَأَنَّ اَ۬للَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿54﴾ كَدَأْبِ ءَالِ
فِرْعَوْنَ وَالَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمْ فَأَهْلَكْنَٰهُم
بِذُنُوبِهِمْ وَأَغْرَقْنَا ءَالَ فِرْعَوْنَ وَكُلٌّ كَانُواْ ظَٰلِمِينَ ﴿55﴾ إِنَّ شَرَّ
اَ۬لدَّوَآبِّ عِندَ اَ۬للَّهِ اِ۬لَّذِينَ كَفَرُواْ فَهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿56﴾ اَ۬لَّذِينَ
عَٰهَدتَّ مِنْهُمْ ثُمَّ يَنقُضُونَ عَهْدَهُمْ فِي كُلِّ مَرَّةٍ وَهُمْ
لَا يَتَّقُونَ ﴿57﴾ فَإِمَّا تَثْقَفَنَّهُمْ فِي اِ۬لْحَرْبِ فَشَرِّدْ بِهِم مَّنْ
خَلْفَهُمْ لَعَلَّهُمْ يَذَّكَّرُونَ ﴿58﴾ وَإِمَّا تَخَافَنَّ مِن قَوْمٍ خِيَانَةً
فَانۢبِذْ إِلَيْهِمْ عَلَىٰ سَوَآءٍ اِنَّ اَ۬للَّهَ لَا يُحِبُّ اُ۬لْخَآئِنِينَ ﴿59﴾ وَلَا تَحْسِبَنَّ
اَ۬لَّذِينَ كَفَرُواْ سَبَقُواْ إِنَّهُمْ لَا يُعْجِزُونَ ﴿60﴾ * وَأَعِدُّواْ لَهُم
مَّا اَ۪سْتَطَعْتُم مِّن قُوَّةٍ وَمِن رِّبَاطِ اِ۬لْخَيْلِ تُرْهِبُونَ
بِهِۦ عَدُوَّ اَ۬للَّهِ وَعَدُوَّكُمْ وَءَاخَرِينَ مِن دُونِهِمْ لَا تَعْلَمُونَهُمُ
اُ۬للَّهُ يَعْلَمُهُمْ وَمَا تُنفِقُواْ مِن شَےْءٍ فِي سَبِيلِ اِ۬للَّهِ
يُوَفَّ إِلَيْكُمْ وَأَنتُمْ لَا تُظْلَمُونَ ﴿61﴾ وَإِن جَنَحُواْ لِلسَّلْمِ
فَاجْنَحْ لَهَا وَتَوَكَّلْ عَلَى اَ۬للَّهِ إِنَّهُۥ هُوَ اَ۬لسَّمِيعُ اُ۬لْعَلِيمُ ﴿62﴾

ربع

54. Wancananka (azabtarwa ga kafirai,) saboda hakika Ubangiji ba yajirkita ni'imar daya ni'imta ta a kan mutane, (ya musanya ta ta zama azaba) sai sun jirkita abinda yake kawukansu, (to, su badd ala ni'imar tasu da butulci, kamar yadda kafiran Makka suka musanya ni'imar ciyarwarsu daga yunwa da amintar dasu daga tsoro da aiko Annabi Sallallahu alaihi wasallama, suka musanya tada kafirci da tsare-wa ga buran shiga Musulunci, dayakin muminai). Hakika Ubangiji mai ji ne masani ne.

55. Kamar al'adar Fir'auna da mutanensa, da wadanda suke gabansu, sunkaryatada ayoyin Ubangijinsu, muka halakar dasu saboda zunubansu, muka nutsar da Fir'auna da mutanensa. (Kowane daya daga al'umma mai karyatawa) sunkasance azzalumai.

(YAYA HALIN WANDA YA WARWARE ALKAWARI?)

56. Hakika mafi sharrin dabbobi nan ga Allah, sune wadanda da suka kafirta, su basa bada gaskiya.

57. Sune wadanda kayi alkwari garesu (bazasu taimaki mushirikai ba,) sannan suke ta warware alkwarinsu a kowane Lokaci, su basa tsoron Allah (a cikin yaudararsu).

58. To, idan ka dace dasu a yaki, to, tarwatsa wanda yake bayansu (saboda ka basu kashi,) donsu wa'azantu.

59. In kaji tsoron ha'inci daga mu-tane wadanda sukayi maka alkawari, to, jefar da alkawarinsu izuwa garesu, halin kasancewarka madaidaici, (ai kuyi daidai dasu cikin sanin warware alkawarin (shine ka sanar dasu cewa ka warware alkawarinsu don kadasu tuhunce ka da warware alkawari). Hakika Ubangiji ba yason maha'inta.

(WANNAN TA SAUKA NE A CIKIN WANDA YAKUBUCE DAGA RANAR BADAR)

60. (Ya Muhammadu Sallallahu alaika wasallama) Kadaka zaci wadanda suka kafirta sun tsere mana, Hakika su bazasu tsere mana ba.

(YIN TANAJE - TANAJE SABODA YAKI NA ABOKAN GABA)

61. Ku tanaji duk abinda kuka sami iko na daga karfi (kamar takobi, bindiga, bam, da sauran irinsu) da daure dawaki saboda Allah, a tsorata makiyan Allah dashi kuma makiyanku kafiran Makka da waninsu, da wadansu koma - bayansu baku san su ba, (sune munafikai a da dayahudu da Nasara da "ya" yansu America a yanzu). Abinda kuka ciyar na ko meme ne saboda Allah, za a cika muku sakamakonsa, baza a tauye muku komai ba.

(KARKATA IZUWA AJIYE MAKAMAI DA KARFAFA RAI A CIKIN YAKI)

62. Idan suka karkata izuwa sulhu, wato dakatar dayaki da kudura amana to, sai ka karkata izuwa sulhun, (Ibn Abbas yace; Wannan aya abar shafewa ce da Ayatus - Saifi). Ka dogara bisa Ubangiji. Hakika shi Ubangiji shine mai ji (ga komai) masani (da komai).

وَإِن يُرِيدُوٓاْ أَن يَخْدَعُوكَ فَإِنَّ حَسْبَكَ اَ۬للَّهُۖ هُوَ اَ۬لذِےٓ أَيَّدَكَ
بِنَصْرِهِۦ وَبِالْمُؤْمِنِينَ ﴿63﴾ وَأَلَّفَ بَيْنَ قُلُوبِهِمْۖ لَوْ أَنفَقْتَ مَا فِے اِ۬لْأَرْضِ
جَمِيعاً مَّآ أَلَّفْتَ بَيْنَ قُلُوبِهِمْ وَلَٰكِنَّ اَ۬للَّهَ أَلَّفَ بَيْنَهُمْۖ إِنَّهُۥ عَزِيزٌ
حَكِيمٞۖ ﴿64﴾ يَٰٓأَيُّهَا اَ۬لنَّبِےٓءُ حَسْبُكَ اَ۬للَّهُ وَمَنِ اِ۪تَّبَعَكَ مِنَ
اَ۬لْمُؤْمِنِينَۖ ﴿65﴾ يَٰٓأَيُّهَا اَ۬لنَّبِےٓءُ حَرِّضِ اِ۬لْمُؤْمِنِينَ عَلَى اَ۬لْقِتَالِۖ
إِن يَكُن مِّنكُمْ عِشْرُونَ صَٰبِرُونَ يَغْلِبُواْ مِاْئَتَيْنِۖ وَإِن تَكُن
مِّنكُم مِّاْئَةٞ يَغْلِبُوٓاْ أَلْفاً مِّنَ اَ۬لذِينَ كَفَرُواْ بِأَنَّهُمْ قَوْمٞ
لَّا يَفْقَهُونَۖ ﴿66﴾ اَ۬لَٰنَ خَفَّفَ اَ۬للَّهُ عَنكُمْ وَعَلِمَ أَنَّ فِيكُمْ
ضُعْفاًۖ فَإِن تَكُن مِّنكُم مِّاْئَةٞ صَابِرَةٞ يَغْلِبُواْ مِاْئَتَيْنِۖ وَإِن يَكُن
مِّنكُمْ أَلْفٞ يَغْلِبُوٓاْ أَلْفَيْنِ بِإِذْنِ اِ۬للَّهِۖ وَاللَّهُ مَعَ اَ۬لصَّٰبِرِينَۖ ﴿67﴾
مَا كَانَ لِنَبِےٓءٍ اَن يَكُونَ لَهُۥٓ أَسْرَيٰ حَتَّيٰ يُثْخِنَ فِے اِ۬لْأَرْضِۖ
تُرِيدُونَ عَرَضَ اَ۬لدُّنْي۪اۖ وَاللَّهُ يُرِيدُ اُ۬لْأٓخِرَةَۖ وَاللَّهُ
عَزِيزٌ حَكِيمٞۖ ﴿68﴾ لَّوْلَا كِتَٰبٞ مِّنَ اَ۬للَّهِ سَبَقَ لَمَسَّكُمْ
فِيمَآ أَخَذْتُمْ عَذَابٌ عَظِيمٞۖ ﴿69﴾ فَكُلُواْ مِمَّا غَنِمْتُمْ
حَلَٰلاً طَيِّباًۖ وَاتَّقُواْ اُ۬للَّهَۖ إِنَّ اَ۬للَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞۖ ﴿70﴾

63. In suka nufi su yaudare ka, (dasulhu, domin suyi tanadi saboda kai,) to, haƙiƙa Allah ne ma'ishinka. Allah ne wanda ya ƙarfafe ka da taimakonsa, ya ƙarfafe ka kuma da muminai, (kamar yadda yahudu sukayi wa Musulmi a yanzu).

64. Shine ya ƙarfafe ka da muminai ya tara tsakanin zukatansu. Da zaka ciyar da abinda yake bayan ƙasa bakiɗaya, bazaka tara tsakanin zukatansu ba. Sai dai Allah ne ya tara (tsakaninsu). Haƙiƙa shi mabuwayi ne (a kan al'amarinsa,) gwanine (cikin aikinsa).

65. Ya wannan Annabi (Sallallahu alaika wasallama) Allah ne ma'ishin ka [1], kyma da waɗanda sukabika na daga muminai, (sun ishe ka).

66. Ya wannan Annabi (Sallallahu alaika wasallama) kwaɗaitar da muminai a kan yaƙin (kafirai). In aka sami ashirin daga gareku masu haƙuri, zasu rinjayi metan daga garesu. in aka sami ɗari daga gareku, zasu rinjayi dubu daga waɗanda suka kafirta. Saboda su mutane ne da basa fahintar (hikimar Allah; aka shafe wannan hukunci da faɗinsa);

67. A yanzu Allah ya sawwake muku, yasan haƙiƙa akwai rauni cikin ku. To, in aka sami ɗari daga cikin ku masu dauriya, zasu rinjayi metan nasu, in aka sami dubu naku, zasu rinjayi dubu biyu nasu, da iznin Allah, Allah yana tareda masu haƙuri.

(SHARI'A TANA SAUKA DAIDAI DA RA'AYIN SAYYADINA UMARU ALLAH YA YARDA DASHI)

68. Bazai halatta ga Annabi ya zamo yana da ribatattu ba, saiya kasnanta a cikin kisan kafirai a cikin ƙasa Kuna nufin amfanin duniya (shine ku karɓi fansa,) Allah yananufin sakamakon Lahira a gareku. Ubangiji mabuwayi ne gwani (a cikin aiki, amma wannan abin shafewa ne da faɗinsa, imma a sakesu bayan haka wa imma a fanshe su).

69. Ba don Littafi daga Allah ya rigaya (da halatta muku ganimomi da ribatattu ba,) da azaba maigirma ta kama ku a cikin abinda kuka karɓa (na daga fansar nan).

70. To, Kuci daga abinda kuka ribata halali mai daɗi, kuji tsoron Allah. Ubangiji mai gafara ne mai jinƙai.

1) Wani malami yayiwa wannan aya mum-munar fahinta yace ma'ananta; ya wannan Annabi Allah ne ma'ishinka, ma'ishin wan-dayabika na daga muminai amma ayar far-ko mai cewa shine ya Raƙfafe ka da Tai-makonsa Tareda muminai ta isa raddi a gareshi don wannan ayar ta biyu ma'anarsu daya data ƙorko, Allah shine masani. - Sanajy -.

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيٓءُ قُل لِّمَن فِيٓ أَيْدِيكُم مِّنَ ٱلْأَسْرَىٰٓ إِن يَعْلَمِ
ٱللَّهُ فِي قُلُوبِكُمْ خَيْراً يُؤْتِكُمْ خَيْراً مِّمَّآ أُخِذَ مِنكُمْ وَيَغْفِرْ لَكُمْ
وَٱللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿71﴾ وَإِن يُرِيدُواْ خِيَانَتَكَ فَقَدْ خَانُواْ ٱللَّهَ
مِن قَبْلُ فَأَمْكَنَ مِنْهُمْ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿72﴾ * إِنَّ ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ فِي سَبِيلِ
ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ ءَاوَواْ وَّنَصَرُوٓاْ أُوْلَٰٓئِكَ بَعْضُهُمْ أَوْلِيَآءُ بَعْضٍ
وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَلَمْ يُهَاجِرُواْ مَا لَكُم مِّن وَلَٰيَتِهِم مِّن شَيْءٍ
حَتَّىٰ يُهَاجِرُواْ وَإِنِ ٱسْتَنصَرُوكُمْ فِي ٱلدِّينِ فَعَلَيْكُمُ ٱلنَّصْرُ إِلَّا عَلَىٰ
قَوْمٍ بَيْنَكُمْ وَبَيْنَهُم مِّيثَٰقٌ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿73﴾ وَٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ بَعْضُهُمْ أَوْلِيَآءُ بَعْضٍ إِلَّا تَفْعَلُوهُ تَكُن فِتْنَةٌ فِي ٱلْأَرْضِ
وَفَسَادٌ كَبِيرٌ ﴿74﴾ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ
فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ ءَاوَواْ وَّنَصَرُوٓاْ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُؤْمِنُونَ حَقّاً
لَّهُم مَّغْفِرَةٌ وَرِزْقٌ كَرِيمٌ ﴿75﴾ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنۢ بَعْدُ وَهَاجَرُواْ
وَجَٰهَدُواْ مَعَكُمْ فَأُوْلَٰٓئِكَ مِنكُمْ وَأُوْلُواْ ٱلْأَرْحَامِ بَعْضُهُمْ
أَوْلَىٰ بِبَعْضٍ فِي كِتَٰبِ ٱللَّهِ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمٌ ﴿76﴾

ثمن

71. Ya wannan Annabi (Sallallahu alaika wasallama) ka faɗa ga waɗanda suke hannunka na daga ribatattu, "In Ubangiji yaso alheri a cikin zukatanku (imani da tsarkakewar aiki) zai baku fiye da abinda aka karɓa daga gareku na fansa, (ya ninninka muku shi a duniya yayi muku sakamako a Lahira) ya gafarta zunubanku. Allah mai gafara ne mai jinƙai (a gareku).

72. Idan sun nufi ha'intarka (da abinda suka nufa na magana,) haƙiƙa sun ha'inci Allah da kafirci tun gaban Badar, Allah ya bada damar yi musu azabadaga garesu (a Badar, kisa da ribacewa. To, su saurari irin wannan in sun komo). Allah masanine (da halittarsa,) gwanine (cikin aikinsa).

(ALAƘA TA MUSULUNCI ITACE TAFI SAURAN ALAƘOƘI ƘARFI)

73. Haƙiƙa waɗanda suka bada gaskiya, sukayi hijjira, sukayi jihadi da dukiyoyinsu da kawukansu a cikin inganta addinin Allah, (sune Muhajirai,) da waɗanda suka tattara Annabi Sallallahu alaihi wasallama) suka taimake shi, (sune Ansaru,) waɗancananka ba'alinsu majiɓintan ba'ali ne (a cikin taimako da gado). Waɗanda suka bada gaskiya basuyi hijira ba, bakuda wani abu na jiɓintarsu,' (ba gado tsakanin ku dasu, ba rabo garesu a cikin ganima,) sai sun yi hijjira, (wannan ma abin shafewa ne da ƙarshen wannan sura). In sun nemi taimakon ku cikin addini, to, dole ne a kanku ku taimake su a kan kafirai, sai ko bisa mutane waɗanda alƙawari yake tsakanin ku dasu, (to, kadaku ,taimake su a kansu, da warware alƙawarinsu). Allah masanine da abinda kuke aikatawa.

74. Waɗanda suka kafirta, ba'alinsu waliyyan ba'ali ne, (a cikin taimako da gado, ba gado tsakanin ku dasu,) idan baku aikata jibintar Musulmi da ije kafirai ba, fitina saita auku a cikin ƙasa da ɓarna maigirma.

75. Waɗanda suka bada gaskiya, sukayi hijira, sukayi yaƙi saboda Allah, da waɗanda suka tara Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) suka taimake shi, waɗancananka sune muminai na gaskiya, gafara na garesu da arziki maigirma (a cikin aljanna).

76. Waɗanda suka bada gaskiya bayan marigayen can izuwa imani, sukayi hijira, sukayi jihadi tareda ku, waɗancananka suna daga cikin ku, (ku Mahajirai da Ansaru,) ma'abuta zumunci, ba'alinsu shine mafi cancantada ba'ali a cikin gado, (daga gado da imani da hijira da aka ambata a ayar data rigaya a cikin Littafin Allah, Lauhul -Mahfuzu). Haƙiƙa Ubangiji masani- ne shi da komai, (hikimar gado tana daga ciki).

9 سُورَةُ التَّوْبَةِ مَدَنِيَّةٌ
وَهِيَ مِائَةٌ وَثَلَاثُونَ ءَايَةً 130

بَرَآءَةٞ مِّنَ اَ۬للَّهِ وَرَسُولِهِۦٓ إِلَى اَ۬لذِينَ عَٰهَدتُّم مِّنَ اَ۬لْمُشْرِكِينَ ۝1
فَسِيحُواْ فِے اِ۬لْأَرْضِ أَرْبَعَةَ أَشْهُرٖ وَاعْلَمُوٓاْ أَنَّكُمْ غَيْرُ مُعْجِزِے اِ۬للَّهِ
وَأَنَّ اَ۬للَّهَ مُخْزِے اِ۬لْكَٰفِرِينَ ۝2 وَأَذَٰنٞ مِّنَ اَ۬للَّهِ وَرَسُولِهِۦٓ
إِلَى اَ۬لنَّاسِ يَوْمَ اَ۬لْحَجِّ اِ۬لْأَكْبَرِ أَنَّ اَ۬للَّهَ بَرِےٓءٞ مِّنَ اَ۬لْمُشْرِكِينَ وَرَسُولُهُۥ
فَإِن تُبْتُمْ فَهُوَ خَيْرٞ لَّكُمْ وَإِن تَوَلَّيْتُمْ فَاعْلَمُوٓاْ أَنَّكُمْ غَيْرُ مُعْجِزِے اِ۬للَّهِ
وَبَشِّرِ اِ۬لذِينَ كَفَرُواْ بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ۝3 إِلَّا اَ۬لذِينَ عَٰهَدتُّم
مِّنَ اَ۬لْمُشْرِكِينَ ثُمَّ لَمْ يَنقُصُوكُمْ شَيْـٔاٗ وَلَمْ يُظَٰهِرُواْ عَلَيْكُمْ أَحَداٗ
فَأَتِمُّوٓاْ إِلَيْهِمْ عَهْدَهُمُۥٓ إِلَىٰ مُدَّتِهِمُۥٓ إِنَّ اَ۬للَّهَ يُحِبُّ اُ۬لْمُتَّقِينَ ۝4
ربع
* فَإِذَا اَ۪نسَلَخَ اَ۬لْأَشْهُرُ اُ۬لْحُرُمُ فَاقْتُلُواْ اُ۬لْمُشْرِكِينَ حَيْثُ وَجَدتُّمُوهُمْ
وَخُذُوهُمْ وَاحْصُرُوهُمْ وَاقْعُدُواْ لَهُمْ كُلَّ مَرْصَدٖ فَإِن تَابُواْ وَأَقَامُواْ
اُ۬لصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُاْ اُ۬لزَّكَوٰةَ فَخَلُّواْ سَبِيلَهُمُۥٓ إِنَّ اَ۬للَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ۝5
وَإِنْ أَحَدٞ مِّنَ اَ۬لْمُشْرِكِينَ اَ۪سْتَجَارَكَ فَأَجِرْهُ حَتَّىٰ يَسْمَعَ كَلَٰمَ
اَ۬للَّهِ ثُمَّ أَبْلِغْهُ مَأْمَنَهُۥ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ قَوْمٞ لَّا يَعْلَمُونَ ۝6

Suratul Taubati

A Madina Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Darī Da Talatin (130)

(WARWARE ALƘAWURAN MUSHIRIKAI DA SANAR DASU YAƘI TAREDA BUWAYA A GARESU)

Ba a rubuta Bismilla a kan wannan sura ba saboda Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama bai umarni dayin haka ba, tamfar yadda Hakimu ya ruwa ito.Hikimar haka tana fahintar da cewa Bismilla wato amintarwa ce, ita ko ta sauka da ɗage amintarwa ne da kansakali, Huzaifatu yana cewa, kuna ambaton ta Suratul Taubati, alhali ita surar azaba ce.

1. Kuɓutar Allah da ma'aikinsa (Sallallahu alaihi wasallama) izuwa waɗanda kayi alƙawari dasu na daga mushirikai.
2. To, kuyi yawo amintattu, (ku mushirikai!) a cikin ƙasa wata hudu, (Zul - ƙaada, Zul - hijja, Maharram, Rajab, to, bakuma amincewa gareku bayan ta,) kuma ku sani, haƙiƙa ku bazaku tserewa Allah ba, (azabarsa,) haƙiƙa Allah mai kunyatar da kafirai ne (a duniya da kisa, a Lahira da wuta).

SHELA!

3. Sanarwa daga Allah da ma'aikinsa izuwa mutane, (wato shela,) ranar Hajji mafi girma, (wato ranar idin babbar salla,) haƙiƙa Ubangiji makuɓuci ne daga mushirikai (da alƙawarinsu) shima maKuɓuci ne (ga buran mushirikai da alƙawuransu, Sayyadina Rasulullahi ya aiki Sayyadina Ali, shekara tara da hijira, yayi shela ran salla a Mina da Waɗannan ayoyi: "Kuma kada mushiriki ya ƙara zuwa hajji bayan wannan shekara, Kada matsiraici Yakuma (ɗawafi a daƙin Allah". Buhari ya ruwa ito shi). To, in kun tuba (daga kafirci,) to, shi, shi yafi alheri a gareku, in kun bada baya (ga buran imani,) ku sani haƙiƙa ku bazaku tserawa Allah ba, yi wa waɗanda suka kafirta bushara da azaba mai raɗadi (kisa da ribacewa a duniya da dawwama a wuta a Lahira).
4. Sai waɗanda kukayi alƙawari dasu daga mushirikai, sannan basu tauye muku komai ba (na sharuɗan alƙawari,) basu taimaki wani kafiri a kanku ba, to, ku cika alƙawarinsu a garesu har izuwa karewar Lokacinsu. Haƙiƙa Allah yana son masu tsoron Allah (da cika alƙawari).

(WAJABCIN YAƘIN MUSHIRIKAI)

5. Idan watanni masu alfarma suka ƙare, to, ku kashe mushirikai inda duk kuka same su. (a cikin hillu ko a cikin haramu) ku datse su, (cikin sansani ko birane, har su bukatu izuwa kisa ko Musulunta,) a zaune musu kowace madakata, in suka tuba (daga kafirci, suka tsayar da salla, suka bada zakka, to, kurabu dasu, haƙiƙa Ubangiji mai gafara ne mai jinƙai (ga wanda ya tuba).

(SASSAUTAWAR MUSULUNCI A CIKIN MA'AMALA DA MUSHIRIKAI)

6. Idan ɗaya daga mushirikai ya nemi ka amintar dashi, to, sai ka amintar dashi, har yaji alƙur'ani, sannan ka iyar dashi wurin amincinsa, (wato gidan mutanensa in bai bada gaskiya ba, don yayi tunani cikin al'amarinsa,) wannan abin ambato saboda haƙiƙa su mutane ne basu san (addinin Allah basuna bukata suji Alƙur'ani).

(SABABIN KUBLTA DAGA ALƘAWURANSU)

كَيْفَ يَكُونُ لِلْمُشْرِكِينَ عَهْدٌ عِندَ اللَّهِ وَعِندَ
رَسُولِهِۦٓ إِلَّا الَّذِينَ عَاهَدتُّمْ عِندَ الْمَسْجِدِ الْحَرَامِ
فَمَا اسْتَقَامُوا لَكُمْ فَاسْتَقِيمُوا لَهُمْ إِنَّ اللَّهَ يُحِبُّ
الْمُتَّقِينَ ﴿7﴾ كَيْفَ وَإِن يَظْهَرُوا عَلَيْكُمْ لَا يَرْقُبُوا فِيكُمْ
إِلًّا وَلَا ذِمَّةً يُرْضُونَكُم بِأَفْوَاهِهِمْ وَتَأْبَىٰ
قُلُوبُهُمْ وَأَكْثَرُهُمْ فَاسِقُونَ ﴿8﴾ اشْتَرَوْا بِآيَاتِ
اللَّهِ ثَمَنًا قَلِيلًا فَصَدُّوا عَن سَبِيلِهِۦٓ إِنَّهُمْ سَاءَ مَا كَانُوا
يَعْمَلُونَ ﴿9﴾ لَا يَرْقُبُونَ فِي مُؤْمِنٍ إِلًّا وَلَا ذِمَّةً وَأُولَٰئِكَ
هُمُ الْمُعْتَدُونَ ﴿10﴾ فَإِن تَابُوا وَأَقَامُوا الصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُا الزَّكَوٰةَ
فَإِخْوَانُكُمْ فِي الدِّينِ وَنُفَصِّلُ الْآيَاتِ لِقَوْمٍ يَعْلَمُونَ ﴿11﴾
* وَإِن نَّكَثُوا أَيْمَانَهُم مِّنۢ بَعْدِ عَهْدِهِمْ وَطَعَنُوا فِي دِينِكُمْ ثمن
فَقَاتِلُوا أَئِمَّةَ الْكُفْرِ إِنَّهُمْ لَا أَيْمَانَ لَهُمْ لَعَلَّهُمْ
يَنتَهُونَ ﴿12﴾ أَلَا تُقَاتِلُونَ قَوْمًا نَّكَثُوا أَيْمَانَهُمْ وَهَمُّوا
بِإِخْرَاجِ الرَّسُولِ وَهُم بَدَءُوكُمْ أَوَّلَ مَرَّةٍ أَتَخْشَوْنَهُمْ
فَاللَّهُ أَحَقُّ أَن تَخْشَوْهُ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿13﴾

7. Kaka alƙawari gurin Allah da ma'aikinsa zai kasance ga kafirai, alhali su sun kafirta dasu, sun warware alƙawari? Sai waɗanda kukayi alƙawari dasu nan ga masallaci mai alfarma, (ranar Hudaibiya su ne ƙuraishu,) to, muddan sun tsayar da alƙawari gareku, to, ku tabbata kan cika musu. Haƙiƙa Allah yana son masu tsoronsa, (Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama ya zarce a kan alƙawarinsu, saida suka warware suka taimaki Bani - Bakarin a kan Bani - Huza'ata).
8. Kaka alƙawari zai kasance garesu, in sukayi rinjaye a kanku, bazasu kula da zumunci a cikin ku ba, wala alƙawari, zasu cuce kunc gwargwadon ikonsu, suna yardar daku ,da bakunansu, (saboda zaƙin harshe,) zukatansu suna kin cikawa dashi, yawaicinsu masu warware alƙawari ne.
9, Sun sai ɗan tamani kaɗan na duniya da ayoyin Allah (alƙur'ani, wato sun bar aiki da ita don sha awaice - sha awaice da son zuciyarsu,) suka hana ga buran shiga addininsa, haƙiƙa su abinda suke aikatawa nan ya mugusta.
10. Basa kula da alƙawari, wala zumunci a cikin mumini, waɗancananka sune haƙiƙanin masu shisshigi kawai!

(IRIN YADDA ZAMUYI MA'AMALA DA WAƊANNAN KAFIRAI)

11. To, in suka tuba, suka tsayar da salla, suka bada zakka, to, "yan uwankune a cikin addini. Muna rarrabe ayoyi ga mutane masu sani.
12. Idan sun warware rantse - rantsensu, bayan alƙawuransu, sukayi suka cikin addininku, to, ku yaki shiyagabannin kafirci, haƙiƙa su ba alƙawura garesu, donsu su hanu (ga buran kafirci).

(KWADAITARWA A KAN YAƘIN KAFIRAI)

13. Shin ba kwa yaƙi mutanen da suka warware alƙawuransu ba, sukayi nufi da fitar da Manzo (Sallallahu alaihi wasallama daga Makka, a gidan shawara, wato (Darul - Nadwati) alhali sune suka fara muku dayaƙi marra farko, da suka yaƙi (Huza'atu) kawayen ku tareda (Bani – ɓak arin) Me zai hana ku yake su, ko tsoronsu kuke ji ne? Allah ne ya cancanci ku tsorace shi, in kun kasance muminai.

قَٰتِلُوهُمْ يُعَذِّبْهُمُ ٱللَّهُ بِأَيْدِيكُمْ وَيُخْزِهِمْ وَيَنصُرْكُمْ
عَلَيْهِمْ وَيَشْفِ صُدُورَ قَوْمٍ مُّؤْمِنِينَ ﴿١٤﴾ وَيُذْهِبْ غَيْظَ
قُلُوبِهِمْ وَيَتُوبُ ٱللَّهُ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿١٥﴾
أَمْ حَسِبْتُمْ أَن تُتْرَكُوا۟ وَلَمَّا يَعْلَمِ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ جَٰهَدُوا۟
مِنكُمْ وَلَمْ يَتَّخِذُوا۟ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلَا رَسُولِهِۦ وَلَا ٱلْمُؤْمِنِينَ
وَلِيجَةً وَٱللَّهُ خَبِيرٌۢ بِمَا تَعْمَلُونَ ﴿١٦﴾ مَا كَانَ لِلْمُشْرِكِينَ
أَن يَعْمُرُوا۟ مَسَٰجِدَ ٱللَّهِ شَٰهِدِينَ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِم بِٱلْكُفْرِ أُو۟لَٰٓئِكَ
حَبِطَتْ أَعْمَٰلُهُمْ وَفِى ٱلنَّارِ هُمْ خَٰلِدُونَ ﴿١٧﴾ إِنَّمَا يَعْمُرُ
مَسَٰجِدَ ٱللَّهِ مَنْ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ وَأَقَامَ ٱلصَّلَوٰةَ
وَءَاتَى ٱلزَّكَوٰةَ وَلَمْ يَخْشَ إِلَّا ٱللَّهَ فَعَسَىٰٓ أُو۟لَٰٓئِكَ أَن يَكُونُوا۟ مِنَ
ٱلْمُهْتَدِينَ ﴿١٨﴾ ۞ أَجَعَلْتُمْ سِقَايَةَ ٱلْحَآجِّ وَعِمَارَةَ ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ
كَمَنْ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ وَجَٰهَدَ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ لَا يَسْتَوُۥنَ
عِندَ ٱللَّهِ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٩﴾ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟
وَهَاجَرُوا۟ وَجَٰهَدُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ أَعْظَمُ
دَرَجَةً عِندَ ٱللَّهِ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْفَآئِزُونَ ﴿٢٠﴾

ربع

14. Ku yaƙe su, Allah zai musu azaba, ya kashe su da hannun ku, Yakunyatar dasu da ribacewa da rinjaye, ya taimake ku kansu, ya warkar da zukatan mutane muminai, (daga abinda akayi musu, sune Huza'atu).
15. Ya tafi da fushin zukatansu, Allah yana karɓar tuba ga wanda yaga dama, (kamar Abi - Sufiy-ana,) Ubangiji masani ne, gwani ne.

(JARRABAR MUSULMAI DA TSARKAKE SU DAGA ZUNUBAI)

16. Haba! kuna zato abar ku, Allah bai nuna waɗanda sukayi yaƙi a cikin ku bada tsarkakewa. Basu riƙi ba sake ciki wanin Allah da ma'aikinsa da muminai ba? Allah mai cikakken sanine da abinda kuke aikatawa.

(RAYA MASALLACI NA MUSULMI NE BAKAFIRAI BA)

17. Bazai yiwu ga mushirikai su raya masallatan Allah ba, suna masu shaidarwa bisa kawukansu da kafirci, waɗancananka aikinsu ya Lalace, (saboda rashin sharaɗin ta, wato Musulunci,) su masu dauwama ne a cikin wuta.
18. Wanda ya bada gaskiya da Allah da ranar lahira, shi kaɗai ne yake raya nasallatan Allah, ya tsayar da salla kyam, ya bada zakka, bai ji tsoron kowa ba sai Allah, to, waɗannan ana kauna su kasance cikin shiryayyu.

(FALALAR IMANI DA JIHADI)

19. Kwa sanya shayar da alhazai da raya masallaci mai alfarma, (wato masu wannan aiki,) kamar wanda ya bada gaskiya da Allah da ranar Lahira, yayi ji-hadi saboda Allah? Baza suyi daidai wurin Allah ba a falala, Allah baya shiriyar mutane azzalumai. (Ta sauka ne don raddi bisa wanda ya riya wannan, shine Sayyadina Abbas, wanda har yanzu shayarwar a hannunsa take har yau).
20. Waɗanda suka bada gaskiya, sukayi hijira, sukayi jihadi saboda Allah, da dukiyoyinsu da kawukansu, su sukafi girman daraja nan ga Allah, (daga waɗansunsu,) waɗancananka sune kadai marabauta.

يُبَشِّرُهُمْ رَبُّهُم بِرَحْمَةٍ مِّنْهُ وَرِضْوَٰنٍ وَجَنَّـٰتٍ لَّهُمْ فِيهَا
نَعِيمٌ مُّقِيمٌ ﴿21﴾ خَـٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عِندَهُۥٓ أَجْرٌ
عَظِيمٌ ﴿22﴾ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تَتَّخِذُوٓا۟ ءَابَآءَكُمْ وَإِخْوَٰنَكُمْ
أَوْلِيَآءَ إِنِ ٱسْتَحَبُّوا۟ ٱلْكُفْرَ عَلَى ٱلْإِيمَـٰنِ ۚ وَمَن يَتَوَلَّهُم
مِّنكُمْ فَأُو۟لَـٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّـٰلِمُونَ ﴿23﴾ قُلْ إِن كَانَ ءَابَآؤُكُمْ
وَأَبْنَآؤُكُمْ وَإِخْوَٰنُكُمْ وَأَزْوَٰجُكُمْ وَعَشِيرَتُكُمْ
وَأَمْوَٰلٌ ٱقْتَرَفْتُمُوهَا وَتِجَـٰرَةٌ تَخْشَوْنَ كَسَادَهَا
وَمَسَـٰكِنُ تَرْضَوْنَهَآ أَحَبَّ إِلَيْكُم مِّنَ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ
وَجِهَادٍ فِى سَبِيلِهِۦ فَتَرَبَّصُوا۟ حَتَّىٰ يَأْتِىَ ٱللَّهُ بِأَمْرِهِۦ ۗ
وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْفَـٰسِقِينَ ﴿24﴾ ۞ لَقَدْ نَصَرَكُمُ ٱللَّهُ فِى مَوَاطِنَ ثمن
كَثِيرَةٍ ۙ وَيَوْمَ حُنَيْنٍ ۙ إِذْ أَعْجَبَتْكُمْ كَثْرَتُكُمْ فَلَمْ تُغْنِ
عَنكُمْ شَيْـًٔا وَضَاقَتْ عَلَيْكُمُ ٱلْأَرْضُ بِمَا رَحُبَتْ
ثُمَّ وَلَّيْتُم مُّدْبِرِينَ ﴿25﴾ ثُمَّ أَنزَلَ ٱللَّهُ سَكِينَتَهُۥ
عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَعَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ وَأَنزَلَ جُنُودًا لَّمْ تَرَوْهَا
وَعَذَّبَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ۚ وَذَٰلِكَ جَزَآءُ ٱلْكَـٰفِرِينَ ﴿26﴾

21. Ubangijinsu yanayi musu albishir da rahamarsa ɗaga gareshi dayardar Allah, da aljannatai, ni'ima madauwamiya na garesu a cikinta.
22. Madauwama a cikinta har abada, Ubangiji Lada maigirma na gareshi.

(DAUKAKAR MUMINAI GA KAFIRAI DA HADARINTA)

"Wannan aya ta sauka a cikin wanda yabar hijira saboda iyalinsa da cinikinsa"
23. Ya waɗanda suka bada gaskiya kadaku ,riƙi iyayenkuda "yan uwanku ababen daukaka, (wato tsarkake soyayya,) idan sun zaɓi kafirci a kan imani, wanda ya daukake su daga cikin ku, to, waɗancananka sune kaɗai azzalumai.
24. Cene (dasu, "Idan iyayenku, da "ya" yayenku, da "yan" uwanku, da matayenku, da danginku, da dukiyoyi da kuka tsuwurwurce ta, da ciniki da kuke tsoron tazgaronsa, da wuraren zama da kuka yarda da ita, ta kasance mafi soyuwa izuwa gareku daga Allah da ma'aikinsa, dayaƙi cikin inganta addininsa, (ku ka Ki yin hijira saboda da waɗannan, da jihadi,) to, kuyi sauraro har Allah yazoda Lamarinsa. (Barazana ce garesu) Allah baya shiriyar mutane fasiƙai.

(BA MAITAIMAKO SAI ALLAH!)

25. Haƙiƙa Ubangiji yataimake ku a guraran yaƙi masu yawa, (kamar Badar, da ƙuraizatu da Naliru,) ka ambaci ranar Hunainu (zaza ne a tsakanin Makka da Da'ifa, ranar da kuka yaƙi Hawazina a cikin Shawwal, shekara ta takwas daga hijira) yayin da yawan ku ya tsokane muku ido, (ku kace "Baza a rinjaye mu ba a yau don ƙanƙanta, su dubu goma sha biyu ne, kafirai kuma dubu hudu) bata wadatar mukuda komai ga buran ku ba, ƙasa tayi muku kunci tare dayalwarta, sannan kuka girka aguje kuna risɓaɓɓu, (Annabi Sallallahu alaihi wasallama ya tabbata a kan farar Alfadararsa, ba kowa tare dashi sai Abbasu da Abi Sufiyana, Shi Abbas yana rike da Linzaminta, shi Abi Sufiyana yana rike da Likkafarta.
26. Sannan Ubangiji ya saukar da nutsuwarsa bisa Manzansa da muminai, (aka maiso su izuwa Ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wasallama, yayin da Abbas ya kirawo su da izininsa, sukayi yaƙi, ya saukar da rindina da baku gansu ba, ya azabci kafirai (da kisa da ribacewa,) wancananka shine sakamakon kafirai.

ثُمَّ يَتُوبُ اللَّهُ مِنْ بَعْدِ ذَٰلِكَ عَلَىٰ مَنْ يَشَاءُ
وَاللَّهُ غَفُورٌ رَحِيمٌ ﴿27﴾ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُوا إِنَّمَا الْمُشْرِكُونَ
نَجَسٌ فَلَا يَقْرَبُوا الْمَسْجِدَ الْحَرَامَ بَعْدَ عَامِهِمْ هَٰذَا
وَإِنْ خِفْتُمْ عَيْلَةً فَسَوْفَ يُغْنِيكُمُ اللَّهُ مِنْ فَضْلِهِ
إِنْ شَاءَ إِنَّ اللَّهَ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿28﴾ قَاتِلُوا الَّذِينَ
لَا يُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ وَلَا بِالْيَوْمِ الْآخِرِ وَلَا يُحَرِّمُونَ
مَا حَرَّمَ اللَّهُ وَرَسُولُهُ وَلَا يَدِينُونَ دِينَ الْحَقِّ
مِنَ الَّذِينَ أُوتُوا الْكِتَابَ حَتَّىٰ يُعْطُوا الْجِزْيَةَ عَنْ يَدٍ
وَهُمْ صَاغِرُونَ ﴿29﴾ وَقَالَتِ الْيَهُودُ عُزَيْرٌ ابْنُ اللَّهِ
وَقَالَتِ النَّصَارَى الْمَسِيحُ ابْنُ اللَّهِ ذَٰلِكَ قَوْلُهُمْ
بِأَفْوَاهِهِمْ يُضَاهُونَ قَوْلَ الَّذِينَ كَفَرُوا مِنْ قَبْلُ
قَاتَلَهُمُ اللَّهُ أَنَّىٰ يُؤْفَكُونَ ﴿30﴾ اتَّخَذُوا أَحْبَارَهُمْ
وَرُهْبَانَهُمْ أَرْبَابًا مِنْ دُونِ اللَّهِ وَالْمَسِيحَ ابْنَ
مَرْيَمَ وَمَا أُمِرُوا إِلَّا لِيَعْبُدُوا إِلَٰهًا وَاحِدًا
لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ سُبْحَانَهُ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿31﴾

27. Sannan Allah yana karɓar tuba bayan wancananka a bisa wanda yaga dama, Allah mai gafara ne mai rahama.

(KADA MUSHIRIKAI SU SHIGA MASALLACI MAI ALFARMA)

28. Yaku waɗanda suka bada gaskiya mushirikai dai najasa ne kawai, (saboda kazantar badininsu) to, kadasu kusanci masallaci mai alfarma, bayan shekararsu wannan, (shekara ta tara daga hijira) in kun ji tsoron talauci ne (dayankewar cinikansu ga buran ku,) to, da sannu Allah zai wadata ku daga falalarsa in yaga dama, (ya wadata su da buɗe - buɗe da jiziya). Haƙiƙa Ubangiji masanine gwani.

(YAƘIN MA'ABOTA LITTAFI DA ƘARSHENSU)

29. Ku yaƙi waɗanda basa bada gaskiya da Allah da ranar Lahira, (don basu bada gaskiya da Annabi Sallallahu alaihi wasal-lama ba,) basa haramta abinda Allah da ma'aikinsa suka haramta, (kamar giya,) basu shiga addinin gaskiya ba, (wanda ya shafe waninsa na daga addinai, shine addinin Musulunci,) sune waɗanda aka basu Littafi (Yahudu da Nasara,) sai sun bada jiziya, (haraji wandaza a sa musu kowace shekara,) bisa jawuwa, alhali suna wulaƙantattu, (masu jawuwa bisa hukuncin Musulunci).

(MA'ABUTA LITTAFI BASA BAUTAWA ALLAH SOSAI)

30. Yahudu Sukace, "Uzairu ɗan Allah ne", Nasara Sukace, "Masihu (Annabi Isa) ɗan Allah ne", wancananka maganar su ce da bakunansu, Barna dogara gareta, Sudai suna kwatantar faɗin waɗanda suka kafirta ne gabansu, (na daga iyayensu don marin baya,) Allah ya tsine musu albarka! Yaya ake juyar dasu (ga buran ban gaskiya tareda tsawon dalili).

31. Su Yahudu sun riƙi malamansu, Nasara sun riƙi rahibansu, iyayen giji ba Allah ba, yayin da sukabi su (a cikin halatta abinda ya haramta, da haramta abinda ya halatta,) sun riƙi Masihu ɗan Maryama abin bautawa, ba a umarce su bakuwa, cikin Attaura da Linjila, sai dai su bautawa, Ubangiji guda ɗaya, ba abin bautawa da gaskiya sai shi, Tsarki ya tabbata gareshi ga buran abinda bai kamace shi bana shirka.

(KAIDIN NASARA DAYAHUDU GA ADDININ MUSULUNCI)

يُرِيدُونَ أَن يُطْفِـُٔواْ نُورَ ٱللَّهِ بِأَفْوَٰهِهِمْ وَيَأْبَى
ٱللَّهُ إِلَّآ أَن يُتِمَّ نُورَهُۥ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْكَٰفِرُونَ ﴿32﴾
هُوَ ٱلَّذِىٓ أَرْسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلْهُدَىٰ وَدِينِ ٱلْحَقِّ لِيُظْهِرَهُۥ
عَلَى ٱلدِّينِ كُلِّهِۦ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْمُشْرِكُونَ ﴿33﴾
* يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّ كَثِيرًا مِّنَ ٱلْأَحْبَارِ وَٱلرُّهْبَانِ
لَيَأْكُلُونَ أَمْوَٰلَ ٱلنَّاسِ بِٱلْبَٰطِلِ وَيَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ
وَٱلَّذِينَ يَكْنِزُونَ ٱلذَّهَبَ وَٱلْفِضَّةَ وَلَا يُنفِقُونَهَا
فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ فَبَشِّرْهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿34﴾ يَوْمَ يُحْمَىٰ
عَلَيْهَا فِى نَارِ جَهَنَّمَ فَتُكْوَىٰ بِهَا جِبَاهُهُمْ
وَجُنُوبُهُمْ وَظُهُورُهُمْ هَٰذَا مَا كَنَزْتُمْ لِأَنفُسِكُمْ
فَذُوقُواْ مَا كُنتُمْ تَكْنِزُونَ ﴿35﴾ إِنَّ عِدَّةَ ٱلشُّهُورِ
عِندَ ٱللَّهِ ٱثْنَا عَشَرَ شَهْرًا فِى كِتَٰبِ ٱللَّهِ يَوْمَ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضَ مِنْهَآ أَرْبَعَةٌ حُرُمٌ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلْقَيِّمُ
فَلَا تَظْلِمُواْ فِيهِنَّ أَنفُسَكُمْ وَقَٰتِلُواْ ٱلْمُشْرِكِينَ كَآفَّةً
كَمَا يُقَٰتِلُونَكُمْ كَآفَّةً وَٱعْلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلْمُتَّقِينَ ﴿36﴾

حزب

32. Suna nufin su bice hasken Allah, (shari'arsa da hujjojinsa,) da harashensu, Allah baya yarda saiya cika haskensa kawai! Ko da kafirai sun ƙi (wannan).

(ALBISHIR GA MUSULMI DA RINJAYEN MUSULUNCI)

33. Shine wanda ya aiko manzonsa, (Annabi Sallallahu alaihi wasallama) dashiriya, da addinin gaskiya, domin ya rinjayar dashi a kan addinai dukkanta, koda mushirikai sun ƙi (haka).

(MAGUDIN MA'ABUTA LITTAFI WATO YAHUDU

34. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! Haƙiƙa yawaici daga Sufayen Yahudu da Nasara, Lalle suna cin dukiyar mutane da banza, (wato cin hanci a cikin hukunci,) suna hana mutane ga buran addinin Allah. (barzanar hana zakka) da waɗandasuce taskace zinare da azurfa basa ci da ita a cikin tafarkin Allah, (zakka ko alheri), to yi musa albishir da azaba mai raɗaɗi

35. Ranar da ake rurawa a kanta a wutar Jahannama, a lallashe goshinansu da itada kuyaɓunsu, da bayayyakinsu, (a yalwata fatunsu har ta sami mashiga a kanta, a ce dasu) "Wannan shine abinda kuka taskace ga kanku, to, ku ɗanɗani kuɓar ku, (wato sakamakon abinda kuka aikata)".

(BA'ALIN AIKACE -AIKACEN JAHILIYYA)

36. Haƙiƙa ƙirgar watanni na shekara nan ga Allah, wata goma sha biyu ne, a cikin Littafin Allah, (Lauhul - Mahfuzu,) ranar daya halicci sammai da ƙassai, akwai daga gareta guda hudu masu alfarma, (sune Zul -ƙaada, Zul - hijja, Maharram, Rajab,) wancananka haramcin watanni) shine addini da yake tsaye kyam! Kadaku ,zalunci kanku a cikinta, (da sabo, saboda sabo a cikinta yafi girman zunubi,) ku yaƙi mushirikai gabaɗaya a cikin dukkan watanni, tamfar dasuke yaƙin ku gabaɗaya, ku sani haƙiƙa Ubangiji yana tareda masu tsoronsa (da taimako da galaba).

إِنَّمَا ٱلنَّسِيٓءُ زِيَادَةٞ فِي ٱلْكُفْرِ يُضَلُّ بِهِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ
يُحِلُّونَهُۥ عَاماٗ وَيُحَرِّمُونَهُۥ عَاماٗ لِّيُوَاطِـُٔواْ عِدَّةَ مَا حَرَّمَ
ٱللَّهُ فَيُحِلُّواْ مَا حَرَّمَ ٱللَّهُۖ زُيِّنَ لَهُمْ سُوٓءُ أَعْمَالِهِمْۖ
وَٱللَّهُ لَا يَهْدِي ٱلْقَوْمَ ٱلْكَٰفِرِينَۖ (37) يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ مَا لَكُمْ إِذَا قِيلَ لَكُمُ ٱنفِرُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ
ٱثَّاقَلْتُمْ إِلَى ٱلْأَرْضِۖ أَرَضِيتُم بِٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا
مِنَ ٱلْأٓخِرَةِۖ فَمَا مَتَٰعُ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا
فِي ٱلْأٓخِرَةِ إِلَّا قَلِيلٌ (38) إِلَّا تَنفِرُواْ يُعَذِّبْكُمْ عَذَاباً
أَلِيماٗ وَيَسْتَبْدِلْ قَوْماً غَيْرَكُمْ وَلَا تَضُرُّوهُ شَيْـٔاٗۖ
وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٖ قَدِيرٌۖ (39) * إِلَّا تَنصُرُوهُ
فَقَدْ نَصَرَهُ ٱللَّهُ إِذْ أَخْرَجَهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ثَانِيَ
ٱثْنَيْنِ إِذْ هُمَا فِي ٱلْغَارِ إِذْ يَقُولُ لِصَٰحِبِهِۦ
لَا تَحْزَنْ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَنَاۖ فَأَنزَلَ ٱللَّهُ سَكِينَتَهُۥ عَلَيْهِ
وَأَيَّدَهُۥ بِجُنُودٖ لَّمْ تَرَوْهَا وَجَعَلَ كَلِمَةَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ
ٱلسُّفْلَىٰۖ وَكَلِمَةُ ٱللَّهِ هِيَ ٱلْعُلْيَاۖ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٌ (40)

ثمن

37. Jinkirta alfarma wata izuwa wani wata, (kamar yadda a jahiliyya suke yi, idan wata yan tsaya alhali suna cikin yaki sujirkinta alfarmar Maharram izuwa Safar,) kari ne a cikin kafirci, (saboda sun kafirce da hukuncin Allah a ciki, waɗanda suka kafirta) suna bata saboda shi, su halarta wannan jinkiri shekara, su haramta shi shekara, donsuyi dace da halatta watada haramta wata maimakon su ƙirga abinda Allah ya haramta (na daga watanni,) saboda su halatta abinda Allah ya haramta, an kawata musu mummunan aikinsu, suka zace shi kyakkyawa. Allah baya shiriyar mutane kafirai.

(KWADAITARWA A ACIKIN JIHADI DA TSORATARWA GA BURANSA)

yayin da Manzon Allah ya kira mutane izuwa yaƙin Tabuka, sun kasance a cikin, wahala da zafin rana, to, wannan saiya wahalar dasu, sai Allah yace:'

38. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya! (Me ke gareku) idan Ance daku, ku fito a cikin inganta addinin Allah, sai ku nauyaya, ku karkata izuwa hutu a cikin ƙasa! Shin kun yarda ne da rayuwar duniya a maimakon Lahira? Jin dadin duniya bai kasance badangane da amfanin Lahira sai cim, (wato kadan).
39. In bazaku fita ba (tareda Annabi Sallallahu alaihi wasallama, a cikin yaƙi,) zaiyi muku azaba, azaba mai raɗaɗi, zai musanya waɗansu mutane baku ba, bazaku cuci Allah da ma'aikinsa komai ba, (saboda Allah mai taimakon addininsa ne,) Allah mai iko ne bisa komai. (Yana daga cikin ikonsa taimakon Addininsa da Annabinsa).

AL SHIRIMMU

40. In bazaku taimaki Annabi ba (Sallallahu alaihi wasallama,) to, haƙiƙa Allah ya taimake shi, zamanin da waɗanda suka kafirta suka tilasar dashi izuwa fita, (da nufin kisa ko daurewa ko kora, a gidan shawara) na biyun mutum biyu, (Sayyadina Abu-bakar Allah ya kara yarda a gareshi,) zamanin dasu biyu suke cikin kogo, zamanin da yake fada ga abokinsa (Abubakar alhali yace dashi zamanin dayaga digadigan mushirikai, da dayansu ya duba ƙarƙashin di-gadigansa guda biyu dayagan mu). "Kada kayi bakin ciki, hakika Allah yana tareda mu". Allah ya saukar da nutsuwarsa ga Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) ya ƙarfafe shi da runduna wacce baku gan ta ba (ta Mala'iku,) yasanya kalmar waɗanda suka kafirta a ƙasa, kalmar Allah kuwa (kalmar sha-hada) iTace maɗaukakiya, Ubangiji mabuwayi ne gwani ne.

(SHIRYASOJOJIN MUSULUNCI)

انفِرُوا۟ خِفَافًا وَثِقَالًا وَجَٰهِدُوا۟ بِأَمْوَٰلِكُمْ وَأَنفُسِكُمْ
فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ذَٰلِكُمْ خَيْرٌ لَّكُمْ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿41﴾
لَوْ كَانَ عَرَضًا قَرِيبًا وَسَفَرًا قَاصِدًا لَّٱتَّبَعُوكَ وَلَٰكِنۢ بَعُدَتْ
عَلَيْهِمُ ٱلشُّقَّةُ وَسَيَحْلِفُونَ بِٱللَّهِ لَوِ ٱسْتَطَعْنَا لَخَرَجْنَا مَعَكُمْ
يُهْلِكُونَ أَنفُسَهُمْ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ إِنَّهُمْ لَكَٰذِبُونَ ﴿42﴾
عَفَا ٱللَّهُ عَنكَ لِمَ أَذِنتَ لَهُمْ حَتَّىٰ يَتَبَيَّنَ لَكَ
ٱلَّذِينَ صَدَقُوا۟ وَتَعْلَمَ ٱلْكَٰذِبِينَ ﴿43﴾ لَا يَسْتَـْٔذِنُكَ ٱلَّذِينَ
يُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ أَن يُجَٰهِدُوا۟ بِأَمْوَٰلِهِمْ
وَأَنفُسِهِمْ وَٱللَّهُ عَلِيمٌۢ بِٱلْمُتَّقِينَ ﴿44﴾ إِنَّمَا يَسْتَـْٔذِنُكَ ٱلَّذِينَ
لَا يُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ وَٱرْتَابَتْ قُلُوبُهُمْ فَهُمْ
فِى رَيْبِهِمْ يَتَرَدَّدُونَ ﴿45﴾ * وَلَوْ أَرَادُوا۟ ٱلْخُرُوجَ لَأَعَدُّوا۟ ربع
لَهُۥ عُدَّةً وَلَٰكِن كَرِهَ ٱللَّهُ ٱنۢبِعَاثَهُمْ فَثَبَّطَهُمْ
وَقِيلَ ٱقْعُدُوا۟ مَعَ ٱلْقَٰعِدِينَ ﴿46﴾ لَوْ خَرَجُوا۟ فِيكُم مَّا زَادُوكُمْ
إِلَّا خَبَالًا وَلَأَوْضَعُوا۟ خِلَٰلَكُمْ يَبْغُونَكُمُ ٱلْفِتْنَةَ
وَفِيكُمْ سَمَّٰعُونَ لَهُمْ وَٱللَّهُ عَلِيمٌۢ بِٱلظَّٰلِمِينَ ﴿47﴾

41. Ku fita kuna masu nishadi ko marasa nishadi, kuyi yaƙi da dukiyoyinkuda kawunanku saboda Allah, wancananku shi yafi gareku, in kun kasance kun san (cewa shi alheri ne gareku, to, kada kuyi nauyi ga buran fita).

(SASHIN ABINDA YA BAYYANA GA MUNAFUKAI)

Yayin da munafukai sukayi jinkiri ga buran fita yaƙin Tabuka sai Ubangiji yace:

42. Da abinda ka kira su izuwa gareshi dan amfanin duniya ne, makusanci ne, kuma tafiya matsakaiciya, da saisu bika (don neman ganima,) sai dai tafiyar tayi musu nisa ne, (saboda haka sukayi jinkiri,) da sannu zasu rantse da Allah (idan kun komo izuwa garesu,) da mun sami da-mar (fita) da mun fita tareda ku, suna halakar da kansu (da rantsuwar ƙarya,) Allah yasan haƙiƙa su maƙaryata ne (a cikin maganarsu wannan).

"To, da can Annabi Sallallahu alaihi wasallama, yayi wa wadansu mutane izini da jinkirin fita da ijtihadi daga gareshi sai Allah ya saukar da wannan aya don nutsarwa ga zuciyarsa".

43. Allah yayi ma rangwame! Donme kayi musu izini (a cikin jinkiri?) har masu gaskiya a cikin hanzari su bayyana gareka, kuma kasan maƙaryata.

44. Wadanda suka bada gaskiya da Allah da ranar Lahira, bazasu nemi izinin ka ba (a cikin jinkiri ga buran) yaƙi da dukiyoyinsu da kawukansu. Allah masanine da masu jin tsoronsa.

45. Wadanda basu bada gaskiya da Allah da ranar Lahira bane suke neman izininka (a cikin jinkiri,) zukatansu sukayi kokwanto (a cikin addini,) su suna dimuwa a cikin kokwantonsu.

(WANI ABU DAGA DABI'AR MUNAFUKAI MUMMUNA SHINE RARRABAKALMA)

46. Dasun nufi fita tareda kai, dasun yi tanaji gareshi (na kayan fada da guzuri,) sai dai Ubangiji yaki zaburar dasune saboda haka yasanyaya musu guiwa, akace (dasu) "Ku tsuguna tareda tsugunannu (marasa Lafiya da matada ƙananan yara).

47. Dasun fita a cikinku bazasu kara muku komai ba sai barna, da tabar da muminai, da kuma sun yi gaggawa da tafiya da annamimanci (wato gulma,) suna neman fitina gareku (ta wajen jefa kiyayya,) a cikinku akwai masu yawan sauraro garesu, (sauraron karba) Allah masanine da azzalumai.

لَقَدِ ٱبْتَغَوُا۟ ٱلْفِتْنَةَ مِن قَبْلُ وَقَلَّبُوا۟ لَكَ ٱلْأُمُورَ
حَتَّىٰ جَآءَ ٱلْحَقُّ وَظَهَرَ أَمْرُ ٱللَّهِ وَهُمْ كَٰرِهُونَ ﴿48﴾
وَمِنْهُم مَّن يَقُولُ ٱئْذَن لِّى وَلَا تَفْتِنِّىٓ أَلَا فِى ٱلْفِتْنَةِ
سَقَطُوا۟ وَإِنَّ جَهَنَّمَ لَمُحِيطَةٌۢ بِٱلْكَٰفِرِينَ ﴿49﴾
إِن تُصِبْكَ حَسَنَةٌ تَسُؤْهُمْ وَإِن تُصِبْكَ مُصِيبَةٌ يَقُولُوا۟
قَدْ أَخَذْنَآ أَمْرَنَا مِن قَبْلُ وَيَتَوَلَّوا۟ وَّهُمْ فَرِحُونَ ﴿50﴾
قُل لَّن يُصِيبَنَآ إِلَّا مَا كَتَبَ ٱللَّهُ لَنَا هُوَ مَوْلَىٰنَا
وَعَلَى ٱللَّهِ فَلْيَتَوَكَّلِ ٱلْمُؤْمِنُونَ ﴿51﴾ قُلْ هَلْ تَرَبَّصُونَ بِنَآ
إِلَّآ إِحْدَى ٱلْحُسْنَيَيْنِ وَنَحْنُ نَتَرَبَّصُ بِكُمْ أَن يُصِيبَكُمُ
ٱللَّهُ بِعَذَابٍ مِّنْ عِندِهِۦٓ أَوْ بِأَيْدِينَا فَتَرَبَّصُوٓا۟ إِنَّا
مَعَكُم مُّتَرَبِّصُونَ ﴿52﴾ قُلْ أَنفِقُوا۟ طَوْعًا أَوْ كَرْهًا
لَّن يُتَقَبَّلَ مِنكُمْ إِنَّكُمْ كُنتُمْ قَوْمًا فَٰسِقِينَ ﴿53﴾
* وَمَا مَنَعَهُمْ أَن تُقْبَلَ مِنْهُمْ نَفَقَٰتُهُمْ إِلَّآ أَنَّهُمْ كَفَرُوا۟ ثمن
بِٱللَّهِ وَبِرَسُولِهِۦ وَلَا يَأْتُونَ ٱلصَّلَوٰةَ إِلَّا وَهُمْ
كُسَالَىٰ وَلَا يُنفِقُونَ إِلَّا وَهُمْ كَٰرِهُونَ ﴿54﴾

48. Hakika sun nemi fitina (gare ka,) tun gaban zuwan ka Madina, sun juya maka al'amura (a cikin yi maka kaidi da bata ad-dininka,) har taimako yazo, al'amarin Allah (a addininsa) yayi rinjaye, alhali su basuna kauna ba.

(WANI ABU DAGA TA'ADODINSU HAR YAU)

49. Akwai daga garesu wanda yake cewayi min izini (cikin jinkiri,) kadaka fitinance ni, (munafiki ne babbashine Jaddu dan kaisu, Manzon Allah yace dashi kana da sha'awa a cikin bugayya da Banil - Asfari, sai yace, wai shi mai kwadayin mataye ne idan yaga matayen Banil - Asfari bazai iya hakuri ga buran su ba, ya zama ya fada cikin hadari, sai Ubangiji yace):"To, jama'a a cikin fitinar nan sukayi dake, hakika jahannaman mai kewayewa ce da kafirai.

50. Idan wani abu mai kyau ya same ka (kamar nasara da ganima) saita bakanta musu, idan musibata same su, saisu ce, "Da ma hakika mun karbi al'amarinmu (a hannunmu) tun gaban wannan musiba, saisu bada baya suna masu muma (da abinda ya same ka).

51. Cene (dasu) "ba abindazai same mu sai abinda Ubangiji ya rubuta zai same mu, Allah ne mataimakinmu, a bisa Ubangiji;to muminai duk su dogara." ga Allah.

52. Cene, "Ba kwa sauraro da mu sai dayan akiba guda biyu kyawawa (nasara ko shahada,) mu ko muna sauraro Allah ya saukar mukuda azabadaga gareshi, (da wato tsawa daga sama,) ko da hannayenmu, (ai mana izini cikin yakin ku,) to, kuyi sauraro (da mu) hakika mu masu sauraron (akibar kune tareda ku)".

(SAKAMAKON MUNAFUNCI A DUNIYA DA LAHIRA)

53. Cene (dasu) "Ku ciyar a cikin da'ar Allah dayarda ko tilas, Allah bazai karbi abinda kuka ciyar badaga gareku, hakika ku kun kasance mutane ne fasikai".

54. Ba abinda ya hana a karbi abinda suka ciyar daga garesu sai don cewa su sun kofirtada Allah da manzonsa, basu zuwa salla face suna cikin kasala, basa ciyarwa face suna masu ki ga ciyarwar, (Don sun ,a gani kamar biyan bashi ce).

فَلَا تُعْجِبْكَ أَمْوَٰلُهُمْ وَلَا أَوْلَٰدُهُمْ إِنَّمَا يُرِيدُ اللَّهُ لِيُعَذِّبَهُم
بِهَا فِي الْحَيَوٰةِ الدُّنْيَا وَتَزْهَقَ أَنفُسُهُمْ وَهُمْ كَٰفِرُونَ 55
وَيَحْلِفُونَ بِاللَّهِ إِنَّهُمْ لَمِنكُمْ وَمَا هُم مِّنكُمْ وَلَٰكِنَّهُمْ
قَوْمٌ يَفْرَقُونَ 56 لَوْ يَجِدُونَ مَلْجَـًٔا أَوْ مَغَٰرَٰتٍ أَوْ مُدَّخَلًا
لَّوَلَّوْا إِلَيْهِ وَهُمْ يَجْمَحُونَ 57 وَمِنْهُم مَّن يَلْمِزُكَ
فِي الصَّدَقَٰتِ فَإِنْ أُعْطُوا مِنْهَا رَضُوا وَإِن لَّمْ يُعْطَوْا مِنْهَا
إِذَا هُمْ يَسْخَطُونَ 58 وَلَوْ أَنَّهُمْ رَضُوا مَا ءَاتَيٰهُمُ اللَّهُ وَرَسُولُهُ
وَقَالُوا حَسْبُنَا اللَّهُ سَيُؤْتِينَا اللَّهُ مِن فَضْلِهِ وَرَسُولُهُ
إِنَّا إِلَى اللَّهِ رَٰغِبُونَ 59 إِنَّمَا الصَّدَقَٰتُ لِلْفُقَرَآءِ وَالْمَسَٰكِينِ
وَالْعَٰمِلِينَ عَلَيْهَا وَالْمُؤَلَّفَةِ قُلُوبُهُمْ وَفِي الرِّقَابِ
وَالْغَٰرِمِينَ وَفِي سَبِيلِ اللَّهِ وَابْنِ السَّبِيلِ فَرِيضَةً
مِّنَ اللَّهِ وَاللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ 60 * وَمِنْهُمُ الَّذِينَ


يُؤْذُونَ النَّبِيٓءَ وَيَقُولُونَ هُوَ أُذْنٌ قُلْ أُذْنُ خَيْرٍ
لَّكُمْ يُؤْمِنُ بِاللَّهِ وَيُؤْمِنُ لِلْمُؤْمِنِينَ وَرَحْمَةٌ لِّلَّذِينَ ءَامَنُوا
مِنكُمْ وَالَّذِينَ يُؤْذُونَ رَسُولَ اللَّهِ لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ 61

55. Kada dukiyoyinsu da 'ya'yansu su baka sha'awa, (saboda maƙarƙashiya Allah yayi musu da ita,) Allah yana nufin dai ya musu azabane da ita a rayuwar duniya, rawukansu ta fita suna kafirai.

(HAKANA TADODIN MUNAFUKAI)

56. Suna rantsuwa da Allah, haƙiƙa su, Lallai suna cikinku (muminai,) su basa daga cikinku, sai dai su mutane ne masu tsoro (kada kuyi musu yadda kukayi wa mushirikai, suna kare kansu da rantsuwa).
57. Da zasu sami mafaka, ko rami, ko gurin shiga dasun girka aguje izuwa gareshi, alhali suna masu taurin kai (ga buran juyawa).
58. Akwai daga garesu wanda yake Laifanta ka a cikin raba sadakoki,, idan an basu daga gareta saisu yarda, idan ba a basu daga gareta ba sai gasu suna fushi.
59. Da cewa haƙiƙa su sun yarda da abinda Allah ya basu, da manzonsa (na daga ganimomi da makamancinta) sunce, "Allah ne ma'ishinmu, da sannu Allah zai bamu daga falalarsa da manzonsa, (abindazai ishe mu,) haƙiƙa mu masu kwaɗayi ne izuwa Ubangiji, (daya kasance alheri a garesu).

(WAƊANDA AKE BAZAKKA)

60. Haƙiƙa zakkoki abar miƙawa ce izuwa fukara'u, (wato waɗanda basu da komai faufau,) da waɗanda basu da abindazai ishe su (sune masakinu,) da masu ɗawainiya a kan zakka (mai tarowa da mai rabawa da marubuci da makamancinsu,) da ababan tattarawar zukatansu (donsu Musulunta ko Musuluncinsu ya tabbata ko ire - irensu su Musulunta, ko su kare wa Musulmi) da masu waɓe wuyaye (wato masu fansar kansu,) da masu biyan bashi, da masu tsaiwa akan yaƙi da wanda ya sare tafarki, rabo abin kaddarawa daga Allah, Allah masanine (da halitta tasa,) gwanine (a cikin aikinsa, bai halarta a bada ita ga wanin waɗannan mutane takwas ba).

(CUTAR MUNAFUKAI GA ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAM)

61. Akwai daga cikin munafukai waɗanda suke cutar Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama wajen Laifanta shi da feshi da asirinsa,) suna cewa, (idan an hane su ga buran wannan don kada yaji,) "Shi kunne ne (wato wai yanajin dukkan abinda aka faɗa yana karɓa, idan mun rantse masa bamu faɗa ba, sai yagasgata mu,)" Cene (dasu) "Shi kunnen alheri ne gareku, (wato mai jin alheri ne ba mai jin sharri ne ba,) yana bada gaskiya da Allah, yana sallamawa ga muminai (a cikin abinda suka bashi Labari,) shi jinkaine ga waɗanda suka bada gaskiya daga cikin ku, waɗannan dasuke cutar Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallam,) azaba mai raɗaɗi ta tabbata a garesu".

يَحْلِفُونَ بِاللَّهِ لَكُمْ لِيُرْضُوكُمْ وَاللَّهُ وَرَسُولُهُ
أَحَقُّ أَنْ يُرْضُوهُ إِنْ كَانُوا مُؤْمِنِينَ ﴿62﴾ أَلَمْ يَعْلَمُوا أَنَّهُ
مَنْ يُحَادِدِ اللَّهَ وَرَسُولَهُ فَأَنَّ لَهُ نَارَ جَهَنَّمَ خَالِدًا
فِيهَا ذَلِكَ الْخِزْيُ الْعَظِيمُ ﴿63﴾ يَحْذَرُ الْمُنَافِقُونَ أَنْ
تُنَزَّلَ عَلَيْهِمْ سُورَةٌ تُنَبِّئُهُمْ بِمَا فِي قُلُوبِهِمْ قُلِ اسْتَهْزِءُوا
إِنَّ اللَّهَ مُخْرِجٌ مَا تَحْذَرُونَ ﴿64﴾ وَلَئِنْ سَأَلْتَهُمْ لَيَقُولُنَّ
إِنَّمَا كُنَّا نَخُوضُ وَنَلْعَبُ قُلْ أَبِاللَّهِ وَآيَاتِهِ
وَرَسُولِهِ كُنْتُمْ تَسْتَهْزِئُونَ ﴿65﴾ لَا تَعْتَذِرُوا قَدْ كَفَرْتُمْ
بَعْدَ إِيمَانِكُمْ إِنْ يُعْفَ عَنْ طَائِفَةٍ مِنْكُمْ تُعَذَّبْ
طَائِفَةٌ بِأَنَّهُمْ كَانُوا مُجْرِمِينَ ﴿66﴾ الْمُنَافِقُونَ وَالْمُنَافِقَاتُ
بَعْضُهُمْ مِنْ بَعْضٍ يَأْمُرُونَ بِالْمُنْكَرِ وَيَنْهَوْنَ عَنِ
الْمَعْرُوفِ وَيَقْبِضُونَ أَيْدِيَهُمْ نَسُوا اللَّهَ فَنَسِيَهُمْ
إِنَّ الْمُنَافِقِينَ هُمُ الْفَاسِقُونَ ﴿67﴾ وَعَدَ اللَّهُ الْمُنَافِقِينَ
وَالْمُنَافِقَاتِ وَالْكُفَّارَ نَارَ جَهَنَّمَ خَالِدِينَ فِيهَا
هِيَ حَسْبُهُمْ وَلَعَنَهُمُ اللَّهُ وَلَهُمْ عَذَابٌ مُقِيمٌ ﴿68﴾

(WANI ABU DAGA ALAMONIN MUNAFINCI)

62. Suna rantsuwa da Allah, (saboda ku, cikin abinda ya iso gareku ku na cutar manzon Allah Sallallahu alaihi wasallam, cewa su basu faɗa ba) donsu yardar da ku, Allah da manzonsa ne mafi cancanta su yardar dasu, in sun kasance muminai (da gaske).

63. Shin basu sani ba cewa Lamarin duka wanda ya sabawa Allah da manzonsa, to, haƙiƙia wutar jahannama ce sakamakonsa! Mai dauwama a cikinta, wancananka shine kunyata maigirma.

64. Munafukai suna fargaba a sauk-ar dasura ga muminai da zata labarta musu abinda yake cikin zukatansu na munafunci, alhali su suna masu izgili tareda haka, cene (dasu) "Kuyi izgili n, (wannan barazana ce ta Allah garesu). Haƙiƙa Ubangiji mai bayyanawar abinda kuke fargabane (na munafuncin ku).

65. Wallahi idan ka tambaye su (ga izgili n dasuke dakai da ƙur'ani, alhali suna tafe taredakai izuwa Tabuka,) Lalle zasu dinga cewa (suna masuyin hanzari,) "Mu kawai mun kasance muna kutsawa ne muna wasa (a cikin zance don mu yanke tsawon tafarki,)" Cene (dasu) "To, da Allah da ayoyinsa da manzonsa kuka kasance kuke izgili ?

66. "Kada kuyi wani hamzari! Haƙiƙa kun kafirta bayan imaninku, in an yi rangwame ga wata ƙungiya daga gareku, (saboda ihlasinta ta tubanta, kamar Mahshiyu ɗan Himyara) ayi azaba ga waɗansu ƙungiya, saboda haƙiƙa su sun kasance masu zarcewa a kan munafunci da izgili .

(MUNAFUKAI DASUFOFINSU DA SAKAMAKONSU)

67. Munafukai maza da mata, ba'alinsu daga ba'ali suke, (wato sun kama a cikin addini kamar guntattakin abu guda ɗaya,) suna umarni da aikin munkari, suna hani ga buran aikin alheri, suna ƙanƙame hannuwansu (ga buran ciyarwa a cikin ɗa'a,) sun mance Allah! Saboda haka Allah ya mance dasu (daga alherinsa, wato ya barsu,) haƙiƙa munafukai su ne aininhin fasiƙai.

68. Allah ya alƙarwata munafukai maza da matada kafirai shiga wutar jahannama masu dauwama a cikin ta, iTace ma'ishinsu, Allah ya tsine musu albarka! Azaba madauwamiya na garesu.

كَالذِينَ مِن قَبْلِكُمْ كَانُوٓاْ أَشَدَّ مِنكُمْ قُوَّةً وَأَكْثَرَ
أَمْوَٰلًا وَأَوْلَٰدًا فَاسْتَمْتَعُواْ بِخَلَٰقِهِمْ فَاسْتَمْتَعْتُم
بِخَلَٰقِكُمْ كَمَا اَسْتَمْتَعَ اَلذِينَ مِن قَبْلِكُم بِخَلَٰقِهِمْ
وَخُضْتُمْ كَالذِے خَاضُوٓاْ أُوْلَٰٓئِكَ حَبِطَتْ أَعْمَٰلُهُمْ
فِے اِ۬لدُّنْي۪ا وَالَاخِرَةِ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ اُ۬لْخَٰسِرُونَ ﴿69﴾ * أَلَمْ يَأْتِهِمْ
نَبَأُ اُ۬لذِينَ مِن قَبْلِهِمْ قَوْمِ نُوحٍ وَعَادٍ وَثَمُودَ ﴿70﴾ وَقَوْمِ
إِبْرَٰهِيمَ وَأَصْحَٰبِ مَدْيَنَ وَالْمُؤْتَفِكَٰتِ أَتَتْهُمْ رُسُلُهُم
بِالْبَيِّنَٰتِ فَمَا كَانَ اَللَّهُ لِيَظْلِمَهُمْ وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمْ
يَظْلِمُونَ ﴿71﴾ وَالْمُؤْمِنُونَ وَالْمُؤْمِنَٰتُ بَعْضُهُمْ أَوْلِيَآءُ بَعْضٍ
يَأْمُرُونَ بِالْمَعْرُوفِ وَيَنْهَوْنَ عَنِ اِ۬لْمُنكَرِ وَيُقِيمُونَ اَلصَّلَوٰةَ
وَيُؤْتُونَ اَلزَّكَوٰةَ وَيُطِيعُونَ اَللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓ أُوْلَٰٓئِكَ
سَيَرْحَمُهُمُ اُ۬للَّهُ إِنَّ اَللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿72﴾ وَعَدَ اَللَّهُ
اُ۬لْمُؤْمِنِينَ وَالْمُؤْمِنَٰتِ جَنَّٰتٍ تَجْرِے مِن تَحْتِهَا اَلَانْهَٰرُ
خَٰلِدِينَ فِيهَا وَمَسَٰكِنَ طَيِّبَةً فِے جَنَّٰتِ عَدْنٍ
وَرِضْوَٰنٌ مِّنَ اَللَّهِ أَكْبَرُ ذَٰلِكَ هُوَ اَلْفَوْزُ اُ۬لْعَظِيمُ ﴿73﴾

ثمن

69. Kamar wa'danda suke gaban ku, sun kasance mafiya tsananin karfi daga gareku, mafiya yawan dukiyoyi da "ya" yaye sukaji da'di da rabonsu (na duniya,) ku kaji da'di (ku munafukai) da naku rabon (na duniya,) tamfar wa'danda suke gabanku, sukaji 'da'di da rabonsu, ku ka kutsa (a cikin 'barna, dasu ka ga Annabi Sallallahu alaihi wasallam,) irin kutsawarsu. Wa'dancananka aikinsu ya Lalace, a duniya da Lahira, wa'dancananka sune ha'ki'kanin ta'ba'b'bu.

70. Shin Labarin wa'danda suke gabansu bai zo musu ba ne? Mutanen Annabi Nuhu da mutanen Annabi Hudu da mutanen Annabi Salihu.

71. Da mutanen Annabi Ibrahimu da mutanen Annabi Sha'aibu, da mutanen Annabi Lu'du, ababen jirkitarwa, an sanya samunsu 'kasansu, 'kasansu samansu, an halakar da mutanen Annabi Nuhu da ruwan Dufana, Adu da iska bakarara, Samudu da girgizar 'kasa, mutanen Annabi Ibrahimu da sauro, Madayanu da rumfar wuta, Manzanninsu sun zo musu da mu'ujizozi (suka 'karyata su, aka halakar dasu,) Allah bai kasance mai zalunta a garesu ba, (yayi musu azaba bada zunubi ba) sai dai kansu suke zalunta kawai!

(MUMINAI DASUFOFINSU DA SAKAMAKONSU)

72. Muminai maza da mata sashinsu maji'bunta sashine, suna umarni da aikin alheri, suna hani ga bu-ran munkari, suna kyautata salla, suna bada zakka, suna bin Allah da manzonsa, wa'dancananka da sannu Allah zai ji'kansu ha'ki'ka Ubangiji mabuwayi ne, (ba abindazai hana shi ga buran cika alkawarinsa da narkonsa,) wato zartar dasu, Gwani baya ajiye komai sai a wurinsa).

73. Allah ya al'kawarta wa muminai maza da mata aljannatai da 'koramu suke gudana 'kar'kashinta, masu dauwama a cikinta, da mazaunai da'da'da acikin aljannatan zama, yarda daga Allah! Shine mafi girma (daga dukkan wannan,) wancananka shine rabo maigirma.

(MA'AMALAR ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA GA MUMINAI DA KAFIRAI)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيٓءُ جَٰهِدِ ٱلْكُفَّارَ وَٱلْمُنَٰفِقِينَ وَاغْلُظْ
عَلَيْهِمْ وَمَأْوَيٰهُمْ جَهَنَّمُ وَبِئْسَ ٱلْمَصِيرُ ﴿74﴾ يَحْلِفُونَ
بِاللَّهِ مَا قَالُواْ وَلَقَدْ قَالُواْ كَلِمَةَ ٱلْكُفْرِ وَكَفَرُواْ بَعْدَ
إِسْلَٰمِهِمْ وَهَمُّواْ بِمَا لَمْ يَنَالُواْ وَمَا نَقَمُوٓاْ إِلَّآ أَنْ أَغْنَيٰهُمُ
ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ مِن فَضْلِهِۦ فَإِنْ يَتُوبُواْ يَكُ خَيْرًا لَّهُمْ
وَإِن يَتَوَلَّوْاْ يُعَذِّبْهُمُ ٱللَّهُ عَذَابًا أَلِيمًا فِي ٱلدُّنْيَا وَالْأٓخِرَةِ
وَمَا لَهُمْ فِي ٱلْأَرْضِ مِن وَلِيٍّ وَلَا نَصِيرٍ ﴿75﴾ * وَمِنْهُم مَّنْ
عَٰهَدَ ٱللَّهَ لَئِنْ ءَاتَيٰنَا مِن فَضْلِهِۦ لَنَصَّدَّقَنَّ وَلَنَكُونَنَّ
مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿76﴾ فَلَمَّآ ءَاتَيٰهُم مِّن فَضْلِهِۦ بَخِلُواْ بِهِۦ وَتَوَلَّواْ
وَّهُم مُّعْرِضُونَ ﴿77﴾ فَأَعْقَبَهُمْ نِفَاقًا فِي قُلُوبِهِمُۥٓ إِلَيٰ يَوْمِ
يَلْقَوْنَهُۥ بِمَآ أَخْلَفُواْ ٱللَّهَ مَا وَعَدُوهُ وَبِمَا كَانُواْ يَكْذِبُونَ ﴿78﴾
أَلَمْ يَعْلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ سِرَّهُمْ وَنَجْوَيٰهُمْ وَأَنَّ ٱللَّهَ
عَلَّٰمُ ٱلْغُيُوبِ ﴿79﴾ ٱلَّذِينَ يَلْمِزُونَ ٱلْمُطَّوِّعِينَ مِنَ
ٱلْمُؤْمِنِينَ فِي ٱلصَّدَقَٰتِ وَالَّذِينَ لَا يَجِدُونَ إِلَّا جُهْدَهُمْ
فَيَسْخَرُونَ مِنْهُمْ سَخِرَ ٱللَّهُ مِنْهُمْ وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿80﴾

ربع

74. Ya wannan Annabi maigirma, yaƙi kafirai (da kansalaki,) munafukai (da harshe da hujja,) ka kaurara a garesu (a cikin tsawa da kyara,) makomarsu jahannama, tir makoma (ita!).

75. Suna rantsuwa da Allah (su munafukan nan) basu faɗi (abinda ya riske ka na zagi) ba, alhali, kuwa Lalle sun faɗi kalmar kafirci, sun kafirta bayan Musuluncinsu, sun yi nufi da abinda bazasu samu ba, (shine kisan gila da manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama daren Aƙaba, wacce take tsakanin tabuka da Madina yayin komowarsa daga Tabuka, su goma da tsirari sai Ammari ɗan Yasiru ya doki fuskar rakumansu, yayin da sukayi arangama dashi, sai suka koma,) basu ƙi komai ba sai cewa Allah ya wadata su da ma'aikin falalarsu daga falarasa, (ya basu ganima bayan tsananin, bukatuwarsu, to, wannan kuwa baya daga abindaza a ƙi) To, in sun tuba (ga buran munafunci, suka bada gaskiya a kai,) zai zama mafi alheri a garesu, idan sun bada baYakuwa (ga buran imani,) Allah zaiyi musu azaba; azaba mai raɗaɗi, a duniya da Lahira, basu da wani majuɓunci a cikin ƙasa, wala mai hana musu azabar Ubangiji.

(ƘISSAR SA'ALABATU DAN HADIBU AL - ANSARI)

76. Akwai daga garesu wanda yayi alƙawari da Allah, Wallahi idan Allah yabamu daga falalarsa Lalle zamuyi sadaka zamu kasance daga salihai (shine Sa'alabatu dan Hadibu Al - ansari, ya roƙi Annabi Salallahu alaihi wasallama ya roƙa masa Allah ya azurta shi da dukiya dazai bada zakka irin yadda ya kamata, sai Allah ya yalwata masa, saiya yanke ga buran Juma'a da salla cikin jama'a, ya hana zakka tamfar da Allah zai faɗa);

77. Yayin daya basu daga falala tasa, sai sukayi rowa dashi suka juya da baya (ga buran da'ar Allah,) alhali suna masu bujirewa.

78. Sai yasanya ƙarshensu munafunchi a cikin zuciyarsu izuwa ranar da zasu gamu dashi (shine ranar alƙiyama,) saboda sun saɓawa Allah abinda suka alƙawarta masa, kuma saboda zamansu maƙaryata (ya kawo zakka izuwa manzon Allah bay-an nan Sallallahu alaihi wasallama sai yace Ubangiji ya hana ni in karɓa daga gareka, saiya hadu yana hurwa, a kansa da turbaya, sannan yazoda ita izuwa Sayyadina Abubakar bai karɓa ba, sannan ya kawo wa Sayyadina Umaru shima bai karɓa ba, sannan ya kawo wa Sayyadina Usman shima bai karba ba, a zamanin Sayyadina Usman ya mutu).

79. Shin (munafukai) basu sani ba ne, haƙiƙa Allah yasan asirinsu da ganawarsu, kuma haƙiƙa Allah masanin asirin fake ne.

(WANI ABU NA DAGA CUTAR MUNAFUKAI GA MUMINAI DA SAKAMAKONSU)

Yayin da ayar sadaka ta sauka, sai wani mutum yayi sadaka da abu mai yawa, sai munafukai sukace mai riya ne, sai kuma wani mutum yayi sadaka da sa'i wato mudu hudu, sai sukace Ubangiji mawadaci ne ga buran sadakar wannan, sai Allah ya saukar da: - "

80. Waɗannan dasuke Laifanta masu tabarru'i (wato yin alheri) na daga muminai a cikin sadakoki, da waɗanda basa samu sai gwargwadon ikonsu, su dingayi musu izgili , Allah zai saka musu sakamakon izgili n nan daga garesu, azaba mai raɗaɗi ta tabbata a garesu.

اِسْتَغْفِرْ لَهُمْ أَوْ لَا تَسْتَغْفِرْ لَهُمْ إِن تَسْتَغْفِرْ لَهُمْ سَبْعِينَ مَرَّةً
فَلَن يَغْفِرَ اللَّهُ لَهُمْ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ كَفَرُوا بِاللَّهِ وَرَسُولِهِ
وَاللَّهُ لَا يَهْدِي الْقَوْمَ الْفَاسِقِينَ (81) فَرِحَ الْمُخَلَّفُونَ
بِمَقْعَدِهِمْ خِلَافَ رَسُولِ اللَّهِ وَكَرِهُوا أَن يُجَاهِدُوا بِأَمْوَالِهِمْ
وَأَنفُسِهِمْ فِي سَبِيلِ اللَّهِ وَقَالُوا لَا تَنفِرُوا فِي الْحَرِّ قُلْ نَارُ
جَهَنَّمَ أَشَدُّ حَرًّا لَّوْ كَانُوا يَفْقَهُونَ (82) فَلْيَضْحَكُوا
قَلِيلًا وَلْيَبْكُوا كَثِيرًا جَزَآءً بِمَا كَانُوا يَكْسِبُونَ (83)
فَإِن رَّجَعَكَ اللَّهُ إِلَىٰ طَآئِفَةٍ مِّنْهُمْ فَاسْتَأْذَنُوكَ لِلْخُرُوجِ
فَقُل لَّن تَخْرُجُوا مَعِيَ أَبَدًا وَلَن تُقَاتِلُوا مَعِيَ
عَدُوًّا إِنَّكُمْ رَضِيتُم بِالْقُعُودِ أَوَّلَ مَرَّةٍ فَاقْعُدُوا
مَعَ الْخَالِفِينَ (84) * وَلَا تُصَلِّ عَلَىٰ أَحَدٍ مِّنْهُم ثمن
مَّاتَ أَبَدًا وَلَا تَقُمْ عَلَىٰ قَبْرِهِ إِنَّهُمْ كَفَرُوا
بِاللَّهِ وَرَسُولِهِ وَمَاتُوا وَهُمْ فَاسِقُونَ (85)
وَلَا تُعْجِبْكَ أَمْوَالُهُمْ وَأَوْلَادُهُمْ إِنَّمَا يُرِيدُ اللَّهُ
أَن يُعَذِّبَهُم بِهَا فِي الدُّنْيَا وَتَزْهَقَ أَنفُسُهُمْ وَهُمْ كَافِرُونَ (86)

81. Ka nemi gafara a garesu (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama,) ko kaɗaka nema musu gafara, (an bashi zaɓi ne a cikin nema musu gafara ga barinsa sai Annabi yace; An bani zabi saina zaɓi Istigfari - Buhari ya ruwaito shi,) in ka nema musu gafara sau saba'in, to, Allah bazai musu gafara ba, wancananka saboda haƙiƙa su sun kafirtada Allah da manzonsa, Allah baya shiriyar mutane fasiƙai.

(MASU JINKIRI GA BURAN YAƘI)

82. Masu jinkiri (ga buran yaƙin Tabuka,) sun yi farin ciki bayan manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) sun ki suyi yaƙi da dukiyoyinsu da kawukansu sa-boda Allah, sashinsu yace da sashi, "Kadaku ,fita yaƙi cikin zafin rana," Cene, "Wutar Jahannama iTace tafi tsananin zafi (daga Tabuka, abinda yafi su kare tada buran jinkiri) dasun kasance sun fahimci (haka, da basuyi jinkiri ga buran fita ba)".
83. Suyi dariya kaɗan (a duniya,) sayi kuka da yawa (aLahira,) don sakamakon abinda suka kasance suna aikatawa.

(YADDA ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA YAKE MA'AMALA DASHIYAGABANNI MUNAFUKAI)

84. Idan Allah yakomo dakai (daga Tabuka) izuwa ƙungiya daga garesu, (na daga waɗanda suka daƙire daga garesu a Maɗina na munafukai,) suka nemi iznin fita daga gareka (izuwa wani yaƙin,) to, cene (dasu) "Bazaku fita dani ba har abada, bazaku ƙara yaƙin kafirai taredani ba, haƙiƙa ku kun yarda da daƙirewa a marrar farko, to, ku zauna tareda mazauna gida, (sune matada ƙananan yara da waninsu)".yayin da Annabi Sallallahu alaihi wasallama yayi salla a kan ɗan Ubaiyu dan Salula, sai Allah yace: -"
85. Kada kayi salla a kan ɗaya daga cikinsu daya mutu, har abada, kadaka tsaya a kan kabarinsa (don ko ziyara ko addu'a,) haƙiƙa su sunkafirtada Allah da ma'aikinsa sun mutu alhali suna kafirai.
86. Kada dukiyoyinsu su ƙayatar dakai ko "ya" yansu, Allah yana nufi kawai yayi musu azabada ita a duniya, rawukansu ta kwaranye alhali suna kafirai.

(MATSAYIN MUNAFUKAI DAGA YAƘI)

وَإِذَا أُنزِلَتْ سُورَةٌ أَنْ ءَامِنُواْ بِاللَّهِ وَجَاهِدُواْ مَعَ رَسُولِهِ
اِسْتَأْذَنَكَ أُوْلُواْ الطَّوْلِ مِنْهُمْ وَقَالُواْ ذَرْنَا نَكُن مَّعَ الْقَاعِدِينَ ﴿87﴾
رَضُواْ بِأَن يَكُونُواْ مَعَ الْخَوَالِفِ وَطُبِعَ عَلَىٰ
قُلُوبِهِمْ فَهُمْ لَا يَفْقَهُونَ ﴿88﴾ لَكِنِ الرَّسُولُ وَالَّذِينَ ءَامَنُواْ
مَعَهُۥ جَاهَدُواْ بِأَمْوَالِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ وَأُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ الْخَيْرَاتُ
وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ الْمُفْلِحُونَ ﴿89﴾ أَعَدَّ اللَّهُ لَهُمْ جَنَّاتٍ تَجْرِي
مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَارُ خَالِدِينَ فِيهَا ذَٰلِكَ الْفَوْزُ الْعَظِيمُ ﴿90﴾
وَجَآءَ الْمُعَذِّرُونَ مِنَ الْأَعْرَابِ لِيُؤْذَنَ لَهُمْ وَقَعَدَ الَّذِينَ
كَذَبُواْ اللَّهَ وَرَسُولَهُۥ سَيُصِيبُ الَّذِينَ كَفَرُواْ مِنْهُمْ
عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿91﴾ لَّيْسَ عَلَى الضُّعَفَآءِ وَلَا عَلَى الْمَرْضَىٰ
وَلَا عَلَى الَّذِينَ لَا يَجِدُونَ مَا يُنفِقُونَ حَرَجٌ إِذَا نَصَحُواْ
لِلَّهِ وَرَسُولِهِۦ مَا عَلَى الْمُحْسِنِينَ مِن سَبِيلٍ
وَاللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿92﴾ وَلَا عَلَى الَّذِينَ إِذَا مَآ أَتَوْكَ
لِتَحْمِلَهُمْ قُلْتَ لَآ أَجِدُ مَآ أَحْمِلُكُمْ عَلَيْهِ تَوَلَّواْ وَّأَعْيُنُهُمْ
تَفِيضُ مِنَ الدَّمْعِ حَزَنًا أَلَّا يَجِدُواْ مَا يُنفِقُونَ ﴿93﴾

87. Idan sura ta sauka (daga Alƙur'ani) cewa ku bada gaskiya da Allah, kuyi yaƙi tareda manzon Allah, ma'abota wadata daga cikinsu saisu nemi izininka su ce, "Bar mu mu kasance tareda daƙirarru (wato masu kin fita)".

88. Sun yardasu kasance tare dama zauna - gida mata dayara, da irinsu, an yimke a bisa zukatansu, to, su basu fahimtar (alheri).

89. Sai dai Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) da waɗanda suka bada gaskiya tare dashi sun yi yaƙi ne tareda dukiyoyinsu da kawukansu, waɗancananka alhairi sun tabbata garesu (a duniya da Lahi ra,) waɗancananka sune haƙiƙa marabauta.

90. Allah ya tanadar musu aljannatai da ƙoramu take gudana ƙiarƙashinsu, masu dauwama a cikinta, wancananka shine rabo mai girma.

(MASU DAƘIREWA NADAGA LARABAWAN ƘAUYE)

91. Masuyin hanzari na daga Larabawan ƙauye sukazo izuwa manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) don yayi musu izini (na zama saboda uzurmsu,) to, yayi musu izinin, waɗanda suka ƙaryata Allah da manzonsa sai suka zauna (ga buran zuwa don neman hanzari,) da sannu azaba mai raɗaɗi zata sami waɗanda suka kafirta daga cikinsu.

(RAUNANA DA MARASA LAFIYA)

92. Babu Laifi a bisa raunana (kamar tsofaffi,) ko marasa Lafiya, (kamar makafi da kumamu,) ko waɗanda basu sami abinda zasu ciyar a cikin yaƙi ba, (to, ba Laifi garesu a cikin jinkiri ga buran fita yaƙi,) amma idan sun yi nasiha ga Allah da manzansa (a cikin halin zaman su, wato basuyi kwarmato ba, basu sanyaya guiwa ba, basu ƙi yin ɗa'a ba) babu hanya ta riƙo da azaba ga masu kyakkyawan aiki, Ubangiji mai gafara ne (garesu) mai jinƙai (dasu a cikin yalwata musu wan ca -ŋanka).

93. Hakana babu laifi ga waɗannan da idan sun zo maka donka ɗauke su taredakai (izuwa yaƙi sune Bani - Mukarini nan su uku; Ma'akilu, Suwaidu da nu'umanu 'ya'yan Mukarrinu da waɗansu mutun bakwai na Ansaru,) ka ce, "Ni ban sami abinda zan ɗaukaka ku a kansa ba". Sai suka juya idanuwansu tana kwararar hawaye, don baƙin ciki, a kan basu sami abinda zasu ciyar (a cikin yaƙi ba).

(MASU JINKIRI BADA WANI HANZARIBA)

حزب

* إِنَّمَا ٱلسَّبِيلُ عَلَى ٱلَّذِينَ يَسْتَـْٔذِنُونَكَ وَهُمْ أَغْنِيَآءُ
رَضُواْ بِأَن يَكُونُواْ مَعَ ٱلْخَوَالِفِ وَطَبَعَ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ
فَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿94﴾ يَعْتَذِرُونَ إِلَيْكُمْ إِذَا رَجَعْتُمْ إِلَيْهِمْ
قُل لَّا تَعْتَذِرُواْ لَن نُّؤْمِنَ لَكُمْ قَدْ نَبَّأَنَا ٱللَّهُ مِنْ أَخْبَارِكُمْ وَسَيَرَى ٱللَّهُ
عَمَلَكُمْ وَرَسُولُهُۥ ثُمَّ تُرَدُّونَ إِلَىٰ عَالِمِ ٱلْغَيْبِ وَٱلشَّهَادَةِ
فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿95﴾ سَيَحْلِفُونَ بِٱللَّهِ لَكُمْ
إِذَا ٱنقَلَبْتُمْ إِلَيْهِمْ لِتُعْرِضُواْ عَنْهُمْ فَأَعْرِضُواْ عَنْهُمْ
إِنَّهُمْ رِجْسٌ وَمَأْوَاهُمْ جَهَنَّمُ جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ يَكْسِبُونَ ﴿96﴾
يَحْلِفُونَ لَكُمْ لِتَرْضَوْاْ عَنْهُمْ فَإِن تَرْضَوْاْ عَنْهُمْ فَإِنَّ ٱللَّهَ
لَا يَرْضَىٰ عَنِ ٱلْقَوْمِ ٱلْفَاسِقِينَ ﴿97﴾ ٱلْأَعْرَابُ أَشَدُّ كُفْرًا وَنِفَاقًا
وَأَجْدَرُ أَلَّا يَعْلَمُواْ حُدُودَ مَا أَنزَلَ ٱللَّهُ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿98﴾
وَمِنَ ٱلْأَعْرَابِ مَن يَتَّخِذُ مَا يُنفِقُ مَغْرَمًا وَيَتَرَبَّصُ بِكُمُ ٱلدَّوَآئِرَ
عَلَيْهِمْ دَآئِرَةُ ٱلسَّوْءِ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿99﴾ وَمِنَ ٱلْأَعْرَابِ مَن يُؤْمِنُ
بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْآخِرِ وَيَتَّخِذُ مَا يُنفِقُ قُرُبَٰتٍ عِندَ ٱللَّهِ وَصَلَوَٰتِ ٱلرَّسُولِ
أَلَآ إِنَّهَا قُرُبَةٌ لَّهُمْ سَيُدْخِلُهُمُ ٱللَّهُ فِي رَحْمَتِهِۦ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿100﴾

94. Hanyar riƙo da azaba kaɗai ta tabbata ga waɗannan dasuke neman izininka (a cikin daƙirewa,) alhali su mawadata ne, sun yardasu kasance tareda mu zauna - gida, Allah ya yimƙe a bisa zukatansu, to, su basu da ilimi.

(ABINDA YA KASANCE NA AL'AMARIN MASU DAƘIREWA GA BURAN YAƘIN TABUKA, BAYAN KOMOWAR MUMINAI IZUWA GARESU)

95. Suna hanzari izuwa gareka (a cikin jinkiri,) idan kun koma izuwa garesu (daga yaƙi,) cene (dasu) "Kada kuyi hanzari, bazamu gasgata ku ba, haƙiƙa Allah yabamu Labarin haluluwanku, da sannu Allah zai nuna aikinkuda manzansa, sannan a koma daku ,(a tashin alƙiyama) izuwa masanin asirin fake dana sarari, ya baku labarin abinda kuka kasance kuna aikatawa.

96. Da sannu zasu rantse da Allah a gareku, idan kun koma izuwa garesu (daga Tabuka, kuma cewa su ma'azurai ne wato masu uzuri a cikin jinkiri,) don ku bujire ga buransu, (ga barin zargi,) to, kurabu dasu, haƙiƙa su kazanta ne, (saboda munin baɗminsu,) makomarsu jahannama, don sakamako da abinda suka kasance suna aikatawa.

97. Suna rantsuwa gareku don ku yarda dasu, to,,in kun yarda dasu, haƙiƙa Ubangiji bazai yarda ga mutane fasiƙai ba.

ZAMAN ƘAUYE

98. Larabawan ƙauye sun fi tsananin kafirci da munafunci (daga "yan birni, saboda wautarsu da kaurin ɗabi'arsu, da nisan su ga buran jin Alƙur'ani,) mafiyacancanta ne su zamo basu san haddodin abinda Allah ya saukar a bisa manzonsa ba (na daga hukunce - hukunce da shari'o'i,) Allah masanine (da halitarsa) gwani (a cikin aikinsa dasu).

99. Akwai daga Larabawan ƙauye wanda yake riƙon abinda ya ciyar saboda Allah biyan bashi, (saboda shi baya ƙaunar sakamakonsa, yana ciyarwa ne don tsoro, sune Banu Asadin da Gaɗafana) yana dakon masibun zamani a kanku, masibun zama ni a kansu kaɗai suke ba a kanku ba,) Allah mai ji ne masani.

(KASANCEWAR ANNABI MUHAMMADU SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA WASIDA TSAKANINMU DA UBANGIJI)

100. Akwai daga Larabawan ƙauye wanda ya bada gaskiya da Allah da ranar Lahira, (kamar Juhainatu, Muzainatu, Gifaru da Aslamu) yake riƙon abinda yake ciyarwa saboda Allah ibadodi nan ga Allah, da tsanantuwa izuwa addu'o'in Manzon Allah a garesu, To, jama'a haƙiƙa ita nafaƙan nan (wato sadakokin nan) ibada ce garesu mai kusantarwa, da sannu Allah zai shigar dasu cikin rahama tasa (aljanna,) Ubangiji mai gafara ne mai rahama [1].

(FIFIKON MUHAJIRAI DA ANSARU DA WANDA YABISU DA IHSANI

1) (Sawi yace : "Domin shi manzon Allah (S.A.W) shine wasida mafi girma a cikin kowace mas'ala, to, ya wajaba 'a hango shi a cikin dukkan aiki na Allah, domin Ubangiji ya bawtar da mu da tsanantuwa dashi da fadinsa : In kum kasance kuna son Allah, to, kubini sai Allah yaso ku, to duka wanda ya riyacewa shi zai sadu Izuwa yardar Allah, badaya riki manzon Allah (S.A.W) Tsani, Wasida Tsakaninsa da Allah Ta'ala ba, to aikinsa ya taɗe.

وَٱلسَّٰبِقُونَ ٱلْأَوَّلُونَ مِنَ ٱلْمُهَٰجِرِينَ وَٱلْأَنصَارِ وَٱلَّذِينَ
ٱتَّبَعُوهُم بِإِحْسَٰنٍ رَّضِىَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُوا۟ عَنْهُ وَأَعَدَّ لَهُمْ
جَنَّٰتٍ تَجْرِى تَحْتَهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا أَبَدًا ذَٰلِكَ ٱلْفَوْزُ
ٱلْعَظِيمُ ﴿101﴾ * وَمِمَّنْ حَوْلَكُم مِّنَ ٱلْأَعْرَابِ مُنَٰفِقُونَ
وَمِنْ أَهْلِ ٱلْمَدِينَةِ مَرَدُوا۟ عَلَى ٱلنِّفَاقِ لَا تَعْلَمُهُمْ نَحْنُ نَعْلَمُهُمْ
سَنُعَذِّبُهُم مَّرَّتَيْنِ ثُمَّ يُرَدُّونَ إِلَىٰ عَذَابٍ عَظِيمٍ ﴿102﴾
وَءَاخَرُونَ ٱعْتَرَفُوا۟ بِذُنُوبِهِمْ خَلَطُوا۟ عَمَلًا صَٰلِحًا وَءَاخَرَ سَيِّئًا
عَسَى ٱللَّهُ أَن يَتُوبَ عَلَيْهِمْ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿103﴾ خُذْ مِنْ
أَمْوَٰلِهِمْ صَدَقَةً تُطَهِّرُهُمْ وَتُزَكِّيهِم بِهَا وَصَلِّ عَلَيْهِمْ إِنَّ صَلَوَٰتِكَ
سَكَنٌ لَّهُمْ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿104﴾ أَلَمْ يَعْلَمُوا۟ أَنَّ ٱللَّهَ هُوَ
يَقْبَلُ ٱلتَّوْبَةَ عَنْ عِبَادِهِۦ وَيَأْخُذُ ٱلصَّدَقَٰتِ وَأَنَّ ٱللَّهَ
هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ﴿105﴾ وَقُلِ ٱعْمَلُوا۟ فَسَيَرَى ٱللَّهُ
عَمَلَكُمْ وَرَسُولُهُۥ وَٱلْمُؤْمِنُونَ وَسَتُرَدُّونَ إِلَىٰ عَٰلِمِ ٱلْغَيْبِ
وَٱلشَّهَٰدَةِ فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿106﴾ وَءَاخَرُونَ مُرْجَوْنَ لِأَمْرِ ٱللَّهِ
إِمَّا يُعَذِّبُهُمْ وَإِمَّا يَتُوبُ عَلَيْهِمْ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿107﴾

ثمن

101. Maciya ƙwallo na farko sune Mahajirai da Ansam, da waɗanda sukabi su da kyautatawa acikin aiki har izuwa ranar Alƙiyama, Allah ya yarda dasu, sun yarda dashi, ya tanadar musu aljannatai wacce ƙoramu take gudana a ƙarƙashinta, masu dauwama a cikinta har abada, wancananka shine rabo maigirma.

(MUTANE IRI IRI NE)

102. Akwai munafukai daga waɗanda suke daura daku ,Yaku mutanen Madina na daga Larabawan ƙauye, (kamar Asja'u, da Aslamu da Gifaru) daga mutanen cikin Madina ma (akwai munafukai har yau waɗanda sukayi taurinkai a bisa munafunci, bakasan su ba 'Sallallahu alaika wasallama)' mune mukasan su. Da sannu zamuyi musu azaba sau biyu (da kunyata ko kisa a duniya, da azabar ƙabari,) sannan a koma dasu a Lahira izuwa azaba maigirma, (wuta).

103. Waɗansu mutanen sun yi furuci da zunubansu, (kamar daƙirewa,) sun cudanya aiki kyakkyawa (shine yaƙinsu gaban wannan,) da wani kuma mummuna, (shi ne daƙirewarsu,) ana ƙaunar Ubangiji ya karɓi tubarsu, Ubangiji haƙiƙa mai gafara ne mai jinƙai.

(KULAWARSA SALLALLAHU \LAIHI WASALLAMA DA SHA'ANIN AL'UMMA A HALIN RAYUWARSA DA BAYAN KAURANSA)

'Ta sauka ne cikin Abu Lubabatu da waɗansu jama'a da suka daure kawukansu a al'amudan masallaci, yayin da abinda ya sauka cikin masu daƙirewa ya iske su, suka rantse cewa ba mai kwancesu sai Annabi Sallallahu alaihi wasallam, to saiya warware su, sai aka saukar da wannan ayar: "

104. Karɓi sadaka daga dukiyoyinsu da zaka tsarkake su ka kwalle su daga tsatsar zunubai (ya riƙi sulusin dukiyoyinsu, wato ukunniya 1/3,) kayi addu'a a garesu, addu'arka rahama ce a garesu, Ubangiji mai ji ne masani.

(FALALAR TUBADA SADAKA DA AIKI NAGARI)

105. Shin basu sani ba! Haƙiƙa Ubangiji shine yake karɓar tubadaga bayinsa,yake karɓar sadakoki, haƙiƙa Ubangiji shine mai yawan karɓar tuba (bisa bayinsa) mai jinƙai (dasu saboda hak sai mu yawaita. tubada sadaka).

106. Cene (dasu) "Ku aikata abinda kuka ga dama, da sannu Ubangiji zai nuna sakamakon aikinku, ma'aikin Allah sallallahu alaihi wasallama yagani da muminai, da sannu za a mayar daku ,izuwa masanin asirin fake da sarari, ya baku Labari da abinda kuka kasance kuna aikatawa.

(WANI NAU'I NA DAGA MASU DAƘIREWA)

107. Waɗansu daga masu daƙirewa ababen jinkirtawa ne ga buran tuba izuwa umarnin Ubangiji a cikinsu da abinda yaga dama, imma yayi musu azaba, (wato su mutu bada tuba ba,) ko ya karɓi tubansu, Ubangiji masanine (da halittarsa,) gwani (cikin aikinsa dasu, mutum uku ne:Muraratu ɗan Rabi'u da Ka'abu ɗan Maliku, da Hilalu ɗan Umaiyatu, sunyi jinkiri don kasala da karkata izuwa hutu, ba don munafunci ba, da basuyi hanzari ba izuwa Annabi Sallallahu alaihi wasallama, kamar yadda waninsu sukayi aka dakatar da al'amarinsu kwana hamsin, Sahabbai suka kaurace musu, saida tubansu ta sauka bayan nan).

الَّذِينَ اَتَّخَذُواْ مَسْجِداً ضِرَاراً وَكُفْراً وَتَفْرِيقاَۢ بَيْنَ
الْمُؤْمِنِينَ وَإِرْصَاداً لِّمَنْ حَارَبَ اللَّهَ وَرَسُولَهُۥ مِن قَبْلُ
وَلَيَحْلِفُنَّ إِنْ أَرَدْنَا إِلَّا الْحُسْنَىٰ وَاللَّهُ يَشْهَدُ إِنَّهُمْ
لَكَٰذِبُونَ (108) لَا تَقُمْ فِيهِ أَبَداً لَّمَسْجِدٌ اُسِّسَ عَلَى التَّقْوَىٰ
مِنْ أَوَّلِ يَوْمٍ اَحَقُّ أَن تَقُومَ فِيهِ فِيهِ رِجَالٌ يُحِبُّونَ
أَن يَتَطَهَّرُواْ وَاللَّهُ يُحِبُّ الْمُطَّهِّرِينَ (109) أَفَمَنُ اُسِّسَ بُنْيَانُهُۥ
عَلَىٰ تَقْوَىٰ مِنَ اللَّهِ وَرِضْوَانٍ خَيْرٌ اَمْ مَّنُ اُسِّسَ بُنْيَانُهُۥ
عَلَىٰ شَفَا جُرُفٍ هَارٍ فَانْهَارَ بِهِۦ فِي نَارِ جَهَنَّمَ وَاللَّهُ لَا يَهْدِي
الْقَوْمَ الظَّٰلِمِينَ (110) لَا يَزَالُ بُنْيَانُهُمُ الَّذِي بَنَوْاْ رِيبَةً
فِي قُلُوبِهِمْ إِلَّا أَن تَقَطَّعَ قُلُوبُهُمْ وَاللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ (111)
* إِنَّ اللَّهَ اشْتَرَىٰ مِنَ الْمُؤْمِنِينَ أَنفُسَهُمْ وَأَمْوَالَهُم ربع
بِأَنَّ لَهُمُ الْجَنَّةَ يُقَاتِلُونَ فِي سَبِيلِ اللَّهِ فَيَقْتُلُونَ
وَيُقْتَلُونَ وَعْداً عَلَيْهِ حَقّاً فِي التَّوْرَىٰةِ وَالْإِنجِيلِ
وَالْقُرْءَانِ وَمَنَ اَوْفَىٰ بِعَهْدِهِۦ مِنَ اللَّهِ فَاسْتَبْشِرُواْ
بِبَيْعِكُمُ الَّذِي بَايَعْتُم بِهِۦ وَذَٰلِكَ هُوَ الْفَوْزُ الْعَظِيمُ (112)

(MASALLACIN CUTARWA, DONME AKA GINA SHI DA MATSAYIN MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA A GARESHI)

108. Akwai daga garesu wańanda suka riƙi masallaci don cutarwa, (su goma sha biyu ne na muna fukai, donsu cuci masallacin ƙubada kafirci Don sun , gina shi da umarnin Abi Amir Rahibi, donya kasance mafaka gareshi, ya kasance ya tafi don yazoda runduna daga ƙaisara donsu yaƙi Annabi Sallallahu alaihi wasallam,) da rarrabawa tsakanin muminai, (wańanda suke salla a ƙuba. saboda sallar ba'alinsu a masallacinsu,) kuma don sauraro ga wanda yayi yaƙeƙeniya da Allah da manzonsa tun gabanin gininsa (shine Abu Amir wanda aka ambata,) Wallahi zasu rinƙa rantsuwa Wallahi bamu nufi komai da gininsa ba sai alheri, (kyautawa kafirai a cikin ruwa da zafi, dayalwatawa bisa Musulmi,) Allah ya tabbata haƙiƙa su maƙaryata ne a cikin wannan, (sun roƙi Annabi Sallallahu alaihi wasallama yayi salla a cikinsa sai Allah yace;

109. Kada kayi salla a cikinsa har abada, (saiya aiki jama'a suka rushe shi suka ƙone shi, suka sanya wurinsa juji, ake yada mushe a ciki,) Lalle masallaci da aka assasa ginin jigajigansa a kan tsoron Allah tun daga far kon rana da aka sauka (a gidan hijira, shine masallacin ƙuba, inji Buhari) shi yafi cancanta daga gareshi ka tsaya kayi salla, akwai jarumai a cikinsa dasuke son su tsarkaka, Allah yana son masu tsarki. (A cikin sahihin Ibn Huzaimata haƙiƙa Sallallahu alaihi wasallam yazo musu a masallacin ƙuba, yace Ubangiji ya kyautata yabo a gareku a cikin tsarki, wane mai tsarkakewa Ne ku ke tsarki dashi! Sukace Wallahi Ya Rasulallahi bamu san komai ba sai dai akwai wańansu makota namu Yahudawa, sun kasance suna wanke dubura tasu daga gayańi, to muka wanke tamfar dasuke wankewa, Bazzaru yace muna biyarwa duwarwatsu da ruwa, sai Annabi yace shine wannan, na hore ku dashi).

110. Yanzu masallacin da aka tusanta gininsa a kan tsoron Allah da ƙaunar yarda daga gareshi, ko wanda aka tusanta gininsa a kan gefen kwazazzabo, rushasshe, saiya rusa dashi tareda magininsa a cikin wutar jahannama, Allah baya shiriyar mutane az zalumai.

111. Ginin su wanda suka gina bazai gushe ba kokwanto a cikin zukatansu sai dai zukatansu su yanyanke (su mutu,) Allah masanine (da halittarsa,) gwanine (cikin aikinsa dasu).

(MUMINAI MASU CIKAKKEN IMANI WATO SUFAYE)

112. Haƙiƙa Ubangiji ya sayi kawukan muminai daga muminai da dukiyoyinsu (zasu bada ita a cikin da'a tasa, kamar Jihadi,) da cewa haƙiƙa aljanna ta tabbata garesu, (wato shine kuńin!) Suyi yaƙi saboda Allah, su kashe a kashe su, Allah ya alƙawarta wannan alƙawartarwa a kansa, (ya tabbatar dashi tabbatarwa,) a Wanene mafi cikawa da alƙawarinsa daga Allah, kuyi farin ciki da cinikinku wanda kukayi cinikayya dashi, wancananka ciniki shine rabo maigirma.

ٱلتَّٰٓئِبُونَ ٱلۡعَٰبِدُونَ ٱلۡحَٰمِدُونَ ٱلسَّٰٓئِحُونَ ٱلرَّٰكِعُونَ
ٱلسَّٰجِدُونَ ٱلۡأٓمِرُونَ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَٱلنَّاهُونَ عَنِ
ٱلۡمُنكَرِ وَٱلۡحَٰفِظُونَ لِحُدُودِ ٱللَّهِۗ وَبَشِّرِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ﴿113﴾
مَا كَانَ لِلنَّبِيِّ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَن يَسۡتَغۡفِرُواْ
لِلۡمُشۡرِكِينَ وَلَوۡ كَانُوٓاْ أُوْلِي قُرۡبَىٰ مِنۢ بَعۡدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمۡ
أَنَّهُمۡ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَحِيمِ ﴿114﴾ وَمَا كَانَ ٱسۡتِغۡفَارُ إِبۡرَٰهِيمَ
لِأَبِيهِ إِلَّا عَن مَّوۡعِدَةٖ وَعَدَهَآ إِيَّاهُ فَلَمَّا تَبَيَّنَ لَهُۥٓ أَنَّهُۥ عَدُوّٞ
لِّلَّهِ تَبَرَّأَ مِنۡهُۚ إِنَّ إِبۡرَٰهِيمَ لَأَوَّٰهٌ حَلِيمٞ ﴿115﴾ وَمَا كَانَ
ٱللَّهُ لِيُضِلَّ قَوۡمَۢا بَعۡدَ إِذۡ هَدَىٰهُمۡ حَتَّىٰ يُبَيِّنَ لَهُم مَّا يَتَّقُونَۚ
إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٌ ﴿116﴾ إِنَّ ٱللَّهَ لَهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلۡأَرۡضِۖ يُحۡيِۦ وَيُمِيتُۚ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ
مِن وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٖ ﴿117﴾ ۞ لَّقَد تَّابَ ٱللَّهُ عَلَى ٱلنَّبِيِّ ثمن
وَٱلۡمُهَٰجِرِينَ وَٱلۡأَنصَارِ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُ فِي سَاعَةِ
ٱلۡعُسۡرَةِ مِنۢ بَعۡدِ مَا كَادَ تَزِيغُ قُلُوبُ فَرِيقٖ مِّنۡهُمۡ
ثُمَّ تَابَ عَلَيۡهِمۡۚ إِنَّهُۥ بِهِمۡ رَءُوفٞ رَّحِيمٞ ﴿118﴾

113. Sune masu tuba (daga shirka da nifaƙa,) masu tsarkake bauta ga Allah, masu godiya a gareshi (bisa kowane hali,) masu yawo (a cikin duniya saboda inganta sha'ani Allah,) masu ruku'u masu sajada, (wato masu tsayar da salla,) masu umarni da aikin alheri, masu hani ga buran aikin munkari, masu kiyayewa da haddodin Allah, yi wa muminai albishir da aljanna.

NEMAN GAFARA GA MUSHIRIKAI, KUMA YAUSHE NE ALLAH YAKE YIN RƘO BISA ZUNUBI)

Wannan aya ta sauka a kan neman gafara da manzon Allah yayi a kan baffansa Abi - Dalib, da neman gafarar ba'alin Sahabbai ga iyayensu mushirikai'

114. Bai kamata ga Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) da waɗanda suka bada gaskiya su nemi gafara ga mushirikai ba kodasun kasance ma'abuta kusancin zumunci, bayan ya bayyana garesu cewa su haƙiƙa "yan wuta ne, (wato sun mutu a kan kafirci).

ZIKIRIN AMFASU

115. Neman gafarar Annabi Ibrahim (Alaihissalam) bai kasance ba sai daga alƙawari da ya alƙawarta masa shi, (da faɗinsa da sannu zan nema maka gafarar Ubangijina, don kwaɗayin ya Musulunta,) yayin data bayyana gareshi cewa shi maƙiyin Allah ne, (wato ya mutu a kan kafirci,) sai Yakuɓuta daga gareshi, (yabar neman gafarar,) haƙiƙa Annabi Ibrahim (Alaihissalam,) mai yawan ƙanƙan dakai ne (da numfasawa ta tsoron Allah, wato faɗin Ahh!!!, Ahh!!! Ahh!!![1] Mai haƙuri a kan cuta.

116. Allah bai kasance zai ɓatar da mutane bayan ya shiryesu (zuwa Musulunci) ba, saiya bayyana musu abindaza suji tsoronsa dashi (na daga aiki,) haƙiƙa Ubangiji masanine da komai.

117. Haƙiƙa Ubangiji mulkin sammai da ƙassai yana gareshi, yana rayawa yana matarwa, bakuda majubunci ba Allah ba wala mai hana muku azaba.

(TUBADA SHARRUDANTA, GASKIYA DA FALALARTA)

118. Wallahi haƙiƙa Ubangiji ya dauwamar da tuba a bisa manzon Allah (Sallallahu, alaihi wasallama) da muhajurai da ansaru, waɗanda sukabi shi zamanin tsanani (yaƙin Tabuka mutum biyu sun raba ashaliyar dabino mutum goma su hau rakumi ɗaya, wannan ya hau wannan ya sauka, zafi yayi tsanani, har suka sha ruwan tumbi,) bayan zukatan jama'a daga garesu ta kusa ta karkace, (ga buran bin sa izuwa daƙirewa don abinda suke cikinsa na daga tsanani,) sannan Ubangiji ya karɓi tubansu da tabbatarwa, Ubangiji mai tsananin jinƙai ne dasu mai rahama ne.

1) Daganan ne waliyai suka samo zikirinsu na Da-rikatul - Anfasi

وَعَلَى ٱلثَّلَٰثَةِ ٱلَّذِينَ خُلِّفُواْ حَتَّىٰٓ إِذَا ضَاقَتْ عَلَيْهِمُ ٱلْأَرْضُ بِمَا رَحُبَتْ
وَضَاقَتْ عَلَيْهِمْ أَنفُسُهُمْ وَظَنُّوٓاْ أَن لَّا مَلْجَأَ مِنَ ٱللَّهِ إِلَّآ إِلَيْهِ
ثُمَّ تَابَ عَلَيْهِمْ لِيَتُوبُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ﴿119﴾ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَكُونُواْ مَعَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿120﴾
مَا كَانَ لِأَهْلِ ٱلْمَدِينَةِ وَمَنْ حَوْلَهُم مِّنَ ٱلْأَعْرَابِ
أَن يَتَخَلَّفُواْ عَن رَّسُولِ ٱللَّهِ وَلَا يَرْغَبُواْ بِأَنفُسِهِمْ عَن
نَّفْسِهِۦ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ لَا يُصِيبُهُمْ ظَمَأٌ وَلَا نَصَبٌ
وَلَا مَخْمَصَةٌ فِے سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلَا يَطَـُٔونَ مَوْطِئًا يَغِيظُ
ٱلْكُفَّارَ وَلَا يَنَالُونَ مِنْ عَدُوٍّ نَّيْلًا إِلَّا كُتِبَ
لَهُم بِهِۦ عَمَلٌ صَٰلِحٌ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُضِيعُ أَجْرَ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿121﴾
وَلَا يُنفِقُونَ نَفَقَةً صَغِيرَةً وَلَا كَبِيرَةً وَلَا يَقْطَعُونَ وَادِيًا
إِلَّا كُتِبَ لَهُمْ لِيَجْزِيَهُمُ ٱللَّهُ أَحْسَنَ مَا كَانُواْ يَعْمَلُونَ ﴿122﴾
وَمَا كَانَ ٱلْمُؤْمِنُونَ لِيَنفِرُواْ كَآفَّةً فَلَوْلَا نَفَرَ مِن كُلِّ
فِرْقَةٍ مِّنْهُمْ طَآئِفَةٌ لِّيَتَفَقَّهُواْ فِے ٱلدِّينِ وَلِيُنذِرُواْ
قَوْمَهُمْ إِذَا رَجَعُوٓاْ إِلَيْهِمْ لَعَلَّهُمْ يَحْذَرُونَ ﴿123﴾

119. Ya karɓi tuba bisa mutum uku waɗanda aka jinkirtar dasu (ga buran tuba,) har lokacin da ƙasa tayi ƙunci a garesu tare dayalwarta, kawukansu tayi kunci a garesu, (saboda baƙin ciki da jinkirin karɓar tubansu,) suka tabbatacewa ba mafaka daga Allah sai izuwa Allah, sannan yayi musu mawafaka da tuba donsu tuba, Ubangiji shine mai yawan karɓar tuba, mai jinƙai.

120. Yaku waɗanda suka bada gaskiya, kuji tsoron Allah, ku zamo tareda masu gaskiya.

(WAJABCIN YAƘI TAREDA MA'AIKIN ALLAH DA SAKAMA KONSA)

121. Bai kamata ga mutanen Madina da waɗanda suke daura dasu na daga Larabawan ƙauye su daƙire ga buran Manzon Allah (idan za shi yaƙi ba,) wala suyi kwaɗayi da kawukansu ga buran kansa, wancananka hani saboda haƙiƙa su kishirwa bazata samesu ba, wala wahala, wala yunwa a cikin sha'anin Allah, wala suyi durtsa, durtsewa dazai fusata wa kafirai ba, wala su sami abin samu daga magauci, (kisa ko ribacewa) ba, face an rubuta musu aiki nagari dashi, haƙiƙa Ubangiji baya tozarta ladan masu kyakkyawan aiki.

122. Bazasu ciyar a cikinsa nafaƙa ƙarama (koda dabinuwa guda ɗaya) ba, wala babba, bazasu yanke zaza ba, face an rubuta musu wannan, don Allah ya saka musu kyakkyawan abinda suka kasance suna aikatawa.

(NEMAN ILIMI TILAS NE)

Yayin da aka urusta su a kan daƙira, Annabi Sallallahu alaihi wasallama ya aika da ƙungiya ta mayaƙa sai suka fito baƙidaya sai Allah yace: -'

123. Bai kamata ga muminai su fita izuwa yaƙi bakiɗaya ba, donme wata ƙungiyabata fita daga kowace ƙabila badaga garesu, domin su nemi ilimin addini, kuma domin su gargaɗar da mutanensu idan sun dawo daga yaƙi, su sanar dasu abinda suka amfana na daga hukunce -hukunce donsu su tsoraci azabar Allah?

(FUSKANTARWA A CIKIN YAƘIN KAFIRAI)

ربع

* يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قَٰتِلُواْ ٱلَّذِينَ يَلُونَكُم
مِّنَ ٱلْكُفَّارِ وَلْيَجِدُواْ فِيكُمْ غِلْظَةً وَاعْلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ
مَعَ ٱلْمُتَّقِينَ ﴿124﴾ وَإِذَا مَآ أُنزِلَتْ سُورَةٌ فَمِنْهُم مَّن
يَقُولُ أَيُّكُمْ زَادَتْهُ هَٰذِهِۦٓ إِيمَٰنًا فَأَمَّا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ فَزَادَتْهُمْ إِيمَٰنًا وَهُمْ يَسْتَبْشِرُونَ ﴿125﴾
وَأَمَّا ٱلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ فَزَادَتْهُمْ رِجْسًا
إِلَىٰ رِجْسِهِمْ وَمَاتُواْ وَهُمْ كَٰفِرُونَ ﴿126﴾ أَوَلَا يَرَوْنَ
أَنَّهُمْ يُفْتَنُونَ فِى كُلِّ عَامٍ مَّرَّةً أَوْ مَرَّتَيْنِ
ثُمَّ لَا يَتُوبُونَ وَلَا هُمْ يَذَّكَّرُونَ ﴿127﴾ وَإِذَا مَآ أُنزِلَتْ
سُورَةٌ نَّظَرَ بَعْضُهُمْ إِلَىٰ بَعْضٍ هَلْ يَرَىٰكُم مِّنْ أَحَدٍ
ثُمَّ ٱنصَرَفُواْ صَرَفَ ٱللَّهُ قُلُوبَهُم بِأَنَّهُمْ قَوْمٌ
لَّا يَفْقَهُونَ ﴿128﴾ لَقَدْ جَآءَكُمْ رَسُولٌ مِّنْ أَنفُسِكُمْ
عَزِيزٌ عَلَيْهِ مَا عَنِتُّمْ حَرِيصٌ عَلَيْكُم بِٱلْمُؤْمِنِينَ
رَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿129﴾ فَإِن تَوَلَّوْاْ فَقُلْ حَسْبِىَ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ
عَلَيْهِ تَوَكَّلْتُ وَهُوَ رَبُّ ٱلْعَرْشِ ٱلْعَظِيمِ ﴿130﴾

124. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya! Ku yaƙi waɗanda suke kusa daku, na daga kafirai, su samu karfi a cikinku, (wato ku ɗanɗana musu kuɗarsu,) ku tabbatacewa haƙiƙa Ubangiji yana tareda masu jin tsoronsa (da taimako da salaba).

(MUNAFUKAI DAYADDA SUKA FUSKANCI ALƘUR'ANI)

125. Idan aka saukar dasura ta ƙur'ani akwai daga munafukai wanda yake faɗa ga sahabbansa wannenan ku wannan aya ta ƙara masa imani, (ban gaskiya, Ubangiji yace,) Amma waɗanda suka bada gaskiya, to, ta ƙara musu imani (saboda gasgatawarsu da ita,) su suna murna da ita.

126. Amma waɗanda kafirci da rau-nin imani yake cikin zukatansu, to, ta ƙara musu kafirci izuwa kafircinsu, sun mutu alhali su suna kafirai.

(SABABIN FARI DA ANNOBADA MASHASSHARU DA YUNWA DA SAURAN IRINSU)

127. Basa gani cewa su ana jarrabarsu a kowace shekara sau ɗayako sau biyu, da fari da cutuka, da annoba, (kwalara da waninsa,) sannan basa tubadaga sabanninsu, kuma su basa gargaɗuwa!

128. Idan an saukar dasura, wacce ta ambace su, Annabi (Sallallahu alaihi wasallam) ya karanta musu ita, sai ba'alinsu yayi duba zuwa ba'ali, (suna nufin gudu,) su ce wani yana ganinku (in kun tashi! in ba wanda yagansu saisu tashi, in kuwa ana ganinsu saisu zauna,) sannan su juye (a kan kafircinsu,) Allah ya juyar da zukatansu (ga buran shiriya,) saboda cewa su haƙiƙa mutane ne basa fahimtar gaskiya.

(KIRARIN UBANGIJI BISA MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

129. Haƙiƙa manzo yazo muku daga kawukanku, (shi Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallam,) wanda wahalar ku take zama damuwa a gareshi, mai kwaɗayi a kan ku shiriya, mai tsananin jinƙai ga muminai, (mai jinƙai da mumunai da nufin alheri).

130. To, idan sukajuya baya (ga buran imani,) to, cene Allah ne ma'ishina, babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, a gareshi kaɗai na dogara, (ba waninsa ba,) shine Ubangijin Al' arshi maigirma (Ya keɓance shi da ambato saboda shine mafi girman ababen halitta).

10 سُورَةُ يُونُسَ مَكِّيَّةٌ
وَهِيَ مِائَةٌ وَتِسْعُ ءَايَاتٍ 109

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

الٓر تِلْكَ ءَايَٰتُ الْكِتَٰبِ الْحَكِيمِ ﴿1﴾ أَكَانَ لِلنَّاسِ عَجَبًا
أَنْ أَوْحَيْنَا إِلَىٰ رَجُلٍ مِّنْهُمْ أَنْ أَنذِرِ النَّاسَ وَبَشِّرِ الَّذِينَ
ءَامَنُوا أَنَّ لَهُمْ قَدَمَ صِدْقٍ عِندَ رَبِّهِمْ قَالَ الْكَٰفِرُونَ
إِنَّ هَٰذَا لَسَٰحِرٌ مُّبِينٌ ﴿2﴾ * إِنَّ رَبَّكُمُ اللَّهُ الَّذِي خَلَقَ ثمن
السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضَ فِي سِتَّةِ أَيَّامٍ ثُمَّ اسْتَوَىٰ عَلَى الْعَرْشِ
يُدَبِّرُ الْأَمْرَ مَا مِن شَفِيعٍ إِلَّا مِنۢ بَعْدِ إِذْنِهِ ذَٰلِكُمُ اللَّهُ رَبُّكُمْ فَاعْبُدُوهُ
أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ﴿3﴾ إِلَيْهِ مَرْجِعُكُمْ جَمِيعًا وَعْدَ اللَّهِ حَقًّا
إِنَّهُ يَبْدَؤُا الْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُ لِيَجْزِيَ الَّذِينَ ءَامَنُوا وَعَمِلُوا
الصَّٰلِحَٰتِ بِالْقِسْطِ وَالَّذِينَ كَفَرُوا لَهُمْ شَرَابٌ مِّنْ حَمِيمٍ وَعَذَابٌ أَلِيمٌ
بِمَا كَانُوا يَكْفُرُونَ ﴿4﴾ هُوَ الَّذِي جَعَلَ الشَّمْسَ ضِيَاءً وَالْقَمَرَ
نُورًا وَقَدَّرَهُ مَنَازِلَ لِتَعْلَمُوا عَدَدَ السِّنِينَ وَالْحِسَابَ مَا خَلَقَ
اللَّهُ ذَٰلِكَ إِلَّا بِالْحَقِّ يُفَصِّلُ الْآيَٰتِ لِقَوْمٍ يَعْلَمُونَ ﴿5﴾

Suratu Yunusa Alaihissalam

A Makka Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Dari Da tara (109)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabaɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe

(AIKOWARSA IZUWA MUTANE BAKIDAYA DA DAUKAKAR DARAJARSA NAN GA UBANGIJI ADAUKAKIN SARKI - SALLALLA-HU ALAIHI WASALLAMA)

!Akwai munaƙasha ga kafirai a cikin aƙidodinsu na addini a cikin wannan aya, da fuskantarwa izuwa ayoyin Allah dasuke cikin wannan kasancewa ta duniya, da jeranta ba' alin ƙissoshi saboda izina da gargaɗi, da abinda yake shiga tsakanin wannan na daga ɗabi'ar mutum, da kwatanta duniya, da curuwa izuwa kwatanta matsayan ranar alƙiyama, da abinda yake bin wannan na daga abinda yake tabbatar data shi da kwatanta Alƙur'ani da tasirinsa'

1. A.L.R. (Allah ne masani da abinda yake nufi da wannan kama,waɗanna ayoyi ayoyin Alƙur' anine abin kyautatawa.)
2. Yanzu ya kasance mana ki ga mutane cewa munyi wahayi izuwa mutum daga cikinsu, (Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama,) cewa gargaɗi mu-tane (kafirai da azaba,) kayi albishir ga waɗanda suka bada gaskiya, cewa Lalle suna da dunduniyar gaskiya nan ga Ubangijinsu, (ai Lada kyakkyawa na daga abinda suka gabatar na daga ayyuka,) kafirai Sukace, "Wannan Alƙur'ani Lalle tsafi ne mabayyani".

(ALLANTAKAR UBANGIJI M HALITTAR SAMMAI DA ƘASSAIDA KOYA MANA SAN NU - SANNU CIKIN AIYUKA)

3. Haƙiƙa Allah ne Ubangijinku wanda ya halicci sammai da ƙassai a cikin miƙidarin kwana shida, (Ance miƙidari saboda a Lokacin babu rana babu wata, kuma dayaga dama da saiya halicce su cikin ƙiftawar ido, to, bai yi haka ba, don yasanar da mu sannu - sannu). Sannan ya daidaita a kan Al' arshi (daidaito daya kamace shi,) yana shirya al'amari tsakanin halitta, ba wani mai ceto ga wani sai bayan izinin Ubangiji, (a nan waɗansu malamai sun yi kuskure da suka ɗauki Annabi a mazaunin gumaka.,) wancananku mai shirya al' amari shine Ubangijinku, ku kaɗaita shi, kaɗaitawar haƙiƙa. Shin ba kwa wa'azantu ba?

(WANI ABU DAGA DALILAN TASHIN ALƘIYAMA DA SAKAMAKO)

4. Izuwa gareshi komawar ku gaba ɗaya, Allah ya alƙawartar da wannan alƙawartawa, ya tabbatar dashi tabbatarwa, haƙiƙa Ubangiji ne yake ƙagen halitta, sannan yake tashin su bayan sun mutu, donya sakawa waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagari da adalci, waɗanda suka kafirta ruwan sha mai tsananin zafi na garesu, da azaba mai raɗaɗi saboda kafircinsu.

(WANI ABU DAGA MABAYYANAR AYOYINSA)

5. Shine wanda yasanya rana ma' abuciyar ƙyalli, yasanya wata haske, Ya sanyashi (ya ƙaddara shi) masaukai (guda ashirin da takwas, a cikin dare ashirin da takwas na kowane wata, yana ɓuya dare biyu idan wata cika zaiyi ko dare ɗaya idan wata nusan zai yi) don ku sani da wancananka adadin shekaru da Lissafi, Allah bai halicci wancananka ba saida gaskiya, (ba don wasa ba, Allah ya girma ga buran wannan,) yana rarrabe ayoyi filla - filla ga mutane masu tunani masu ilimin haƙiƙa.

إِنَّ فِي اخْتِلَافِ الَّيْلِ وَالنَّهَارِ وَمَا خَلَقَ اللَّهُ فِي السَّمَٰوَٰتِ
وَالْأَرْضِ لَآيَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَتَّقُونَ ﴿6﴾ إِنَّ الَّذِينَ لَا يَرْجُونَ لِقَآءَنَا
وَرَضُوا بِالْحَيَوٰةِ الدُّنْيَا وَاطْمَأَنُّوا بِهَا وَالَّذِينَ هُمْ عَنْ ءَايَٰتِنَا
غَٰفِلُونَ ﴿7﴾ أُولَٰٓئِكَ مَأْوَىٰهُمُ النَّارُ بِمَا كَانُوا يَكْسِبُونَ ﴿8﴾
إِنَّ الَّذِينَ ءَامَنُوا وَعَمِلُوا الصَّٰلِحَٰتِ يَهْدِيهِمْ رَبُّهُم بِإِيمَٰنِهِمْ
تَجْرِي مِن تَحْتِهِمُ الْأَنْهَٰرُ فِي جَنَّٰتِ النَّعِيمِ ﴿9﴾ دَعْوَىٰهُمْ فِيهَا
سُبْحَٰنَكَ اللَّهُمَّ وَتَحِيَّتُهُمْ فِيهَا سَلَٰمٌ وَءَاخِرُ دَعْوَىٰهُمْ أَنِ الْحَمْدُ
لِلَّهِ رَبِّ الْعَٰلَمِينَ ﴿10﴾ ۞ وَلَوْ يُعَجِّلُ اللَّهُ لِلنَّاسِ الشَّرَّ اسْتِعْجَالَهُم بِالْخَيْرِ
لَقُضِيَ إِلَيْهِمْ أَجَلُهُمْ فَنَذَرُ الَّذِينَ لَا يَرْجُونَ لِقَآءَنَا فِي طُغْيَٰنِهِمْ
يَعْمَهُونَ ﴿11﴾ وَإِذَا مَسَّ الْإِنسَٰنَ الضُّرُّ دَعَانَا لِجَنۢبِهِۦٓ أَوْ قَاعِدًا
أَوْ قَآئِمًا فَلَمَّا كَشَفْنَا عَنْهُ ضُرَّهُۥ مَرَّ كَأَن لَّمْ يَدْعُنَآ إِلَىٰ ضُرٍّ مَّسَّهُۥ
كَذَٰلِكَ زُيِّنَ لِلْمُسْرِفِينَ مَا كَانُوا يَعْمَلُونَ ﴿12﴾ وَلَقَدْ أَهْلَكْنَا
الْقُرُونَ مِن قَبْلِكُمْ لَمَّا ظَلَمُوا وَجَآءَتْهُمْ رُسُلُهُم بِالْبَيِّنَٰتِ
وَمَا كَانُوا لِيُؤْمِنُوا كَذَٰلِكَ نَجْزِي الْقَوْمَ الْمُجْرِمِينَ ﴿13﴾
ثُمَّ جَعَلْنَٰكُمْ خَلَٰٓئِفَ فِي الْأَرْضِ مِنۢ بَعْدِهِمْ لِنَنظُرَ كَيْفَ تَعْمَلُونَ ﴿14﴾

ربع

6. Akwai ayoyi a cikin kaikawon dare da rana (da karuwa da raguwa,) akwai ayoyi a cikin abinda Allah ya halitta a cikin sammai (na Mala'ikuda rana da taurari da wanin wannan,) akwai ayoyi a cikin ƙassai, (shine naman daji da duwarwatsu, da koguna da ƙoramu, da itatuwa, da waninta,) ga mutane masu tsoron Allah, (ya ƙeɓance su da ambatonsu masu tsoro ne Don sun ,e masu amfani da ayoyin).

(MUMINI DA KAFIRI DA ƘARSHEN KOWANNE)

7. Haƙiƙa waɗannan da basa tsor-on saduwa da mu (da tashin alƙiyama,) suka yarda da rayuwar duniya, (maimakon Lahira Don sun , yi musun ta,) suka nutsu da ita,da waɗandasu suke marabkana ga ayoyinmu.
8. Waɗancananka makomarsu wuta, saboda abinda suke aikatawa (na mushirikanci da saɓon Allah).
9. Haƙiƙa waɗanda suka bada gaskiya, sukayi aiki nagari, Ubangijinsu yana shiriyarsu saboda imaninsu dashi, yasanya musu haske da zasu shiriya dashi ranar alƙiyama, (shine a suranta musu ayyukansu nagari dasura kyakkyawa yayin fitar su daga ƙaɓurbura, su ce da ma' abucinta, na kasance ina wahal dakai a duniya, to, hau gadon bayana, shine faɗin Ubangiji ranar da muke tara masu tsoron Allah izuwa Ubangiji suna baƙin girma,) ƙoramu suna gudana ƙarƙashinsu a cikin aljannatan ni' ima.
10. Abinda suke marmari a cikinta su ce; Tsarki ya tabbatar maka ya Ubangiji, (yana nufin wannan kalma iTace masaukin Kun - fayakun daga Ubangiji, komai suke so in sunce (SUBUHANA KAL - LAHUMMA) saisu ganshi a gabansu) gaisuwarsu a cikin aljanna SALAMUN (wato assalamu alaikum) ƙarshen abin neman su alhamdu Lillahi Rabbl - alamin, (Allah yasanya mu cikinsu Amin).

(TALALA TA UBANGIJI DA WANI ABU DAGA DABI'O'IN 'YAN ADAM DA TADODINSU)

"Yayin da kafirai suka ƙagara da saukar azabar sai Allah yace:"

11. Da Allah yana gaggawa da sharri ga mutane yadda suke gaggawa da alheri, da an hukunta halakarsu izuwa garesu, (ai da an halakar dasu,) sai dai yayi musujinkiri ne, to, mubar waɗanda basa tsoron saduwa a cikin shisshiginsu suna ɗimuwa.
12. Idan tsanani ko rashin lafiyaya sami kafirai da mai tauyayyen imani saiya kira mu a kashingide ko a zaune ko a tsaye, (a kowane hali,) yayin da muka yaye masa saiya zarce a kan sabonsa kamar bai taɓa kiranmu a kan wani tsanani daya sameshi ba, tamfar da muka ƙawata wa nakisul - imani addu' a yayin sauki, muka ƙawata wa mushirikai abinda suka kasance suna aikatawa.

(AL' ADAR UBANGIJI A CIKIN AL' UMMA)

13. Haƙiƙa mun halakar da tsaraiku na daga gabanku yaku mutanen Makka yayin da sukayi shirka, alhali manzanninsu sun zo musu da hujjoji mabayyana (a kan gaskiyarsu,) basu kasance masu bada gaskiya ba, tamfar da muka halakar da wancananka muke sakawa kafirai.
14. Sannan muka sanya ku (Yaku mutanen Makka!) mana ya a bayansu a kan ƙasa, don mu ga abinda zaku aikata a cikinta, (ko kwayi izna dasu ku gasgata manzanninmu).

وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمُۥٓ ءَايَاتُنَا بَيِّنَٰتٖ قَالَ ٱلَّذِينَ
لَا يَرْجُونَ لِقَآءَنَا ٱئْتِ بِقُرْءَانٍ غَيْرِ هَٰذَآ أَوْ بَدِّلْهُ
قُلْ مَا يَكُونُ لِيَ أَنُ ابَدِّلَهُۥ مِن تِلْقَآءِيْ نَفْسِيَ إِنَ اتَّبِعُ إِلَّا مَا يُوحَىٰٓ
إِلَيَّ إِنِّيَ أَخَافُ إِنْ عَصَيْتُ رَبِّي عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٖ ﴿15﴾
قُل لَّوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَا تَلَوْتُهُۥ عَلَيْكُمْ وَلَآ أَدْرَىٰكُم بِهِۦ فَقَدْ
لَبِثْتُ فِيكُمْ عُمُرًا مِّن قَبْلِهِۦٓ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿16﴾ فَمَنَ اَظْلَمُ
مِمَّنِ اِفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَوْ كَذَّبَ بِـَٔايَٰتِهِۦٓ
إِنَّهُۥ لَا يُفْلِحُ ٱلْمُجْرِمُونَ ﴿17﴾ وَيَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ
مَا لَا يَضُرُّهُمْ وَلَا يَنفَعُهُمْ وَيَقُولُونَ هَٰٓؤُلَآءِ شُفَعَٰٓؤُنَا عِندَ ٱللَّهِ
قُلْ أَتُنَبِّـُٔونَ ٱللَّهَ بِمَا لَا يَعْلَمُ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِي ٱلْأَرْضِ
سُبْحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿18﴾ * وَمَا كَانَ
ٱلنَّاسُ إِلَّآ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ فَٱخْتَلَفُواْ وَلَوْلَا كَلِمَةٞ
سَبَقَتْ مِن رَّبِّكَ لَقُضِيَ بَيْنَهُمْ فِيمَا فِيهِ
يَخْتَلِفُونَ ﴿19﴾ وَيَقُولُونَ لَوْلَآ أُنزِلَ عَلَيْهِ ءَايَةٞ مِّن رَّبِّهِۦ
فَقُلْ إِنَّمَا ٱلْغَيْبُ لِلَّهِ فَٱنتَظِرُوٓاْ إِنِّي مَعَكُم مِّنَ ٱلْمُنتَظِرِينَ ﴿20﴾

ثمن

(WANI ABU DAGA KAIDUN MUSHIRIKAI DA RADDI A KANSA)

15. Idan ana karantawar ayoyinmu (na ƙur' ani) a garesu mabayyana, waɗanda basa tsoron saduwa da mu saisu ce, "Zoda wani Alƙur'ani ba wannan ba (wanda babu laifanta iyayen gijinmu, a cikinsa,) ko ka musanyashi (da kanka,) Cene (dasu) "Bazai yiwu gare ni in musanyashi da kaina ba, ni bana bi sai abinda aka aiko izuwa gareni, ni ina jin tsoron rana maigirma (iTace alƙiyama in na sabawa Ubangijina)".

16. Cene "Da Allah yaga dama da bazan karanta shi a gareku, ba, da bazai sanar daku, shi ba, haƙiƙa na zauna a cikinku she-kara arba'in gabansa ban taɓa cewa daku, komai ba, shin to, ba kwa hankalci (cewa shi Alƙur'ani badaga gareni) ba ne".

17. Ba mafi zalunci daga wanda ya ƙirƙiri ƙarya bisa Ubangiji ko ya ƙaryatada ayoyinsa (Alƙur' ani) haƙiƙa al'amarin mushirikai bazasu rabauta ba.

(WANI ABU DAGA SURORIN SHIRKA A JAHILIYYA)

18. Suna bautawa ba Allah ba abinda bazai cuce su (in basu bauta masa) ba, bazai amfane su ba (in sun bauta masa, shine gumaka) suna faɗa daga gareta ita gumaka, waɗannan sune masu cetonmu wurin Allah, Cene (dasu) "Yaya zaku ba wa Allah Labari da abinda bai sani ba a cikin sammai da ƙassai. Tsarki ya tabbatar masa, ya girma ga buran abinda suke shirkanta shi (taredashi)".

(HALITAR ALLAH)

19. Mutane basu kasance ba sai al' umma ɗaya (a kan addini ɗaya shine addinin Islam tun daga Annabi Adam Alaihissalam izu-wa Nuhu Alaihissalam,) to, suka sassaɓa (shine waɗansu ba'ali suka tabbata kan Musulunci, wasu ba'ali suka kafirta,) ba don kalma data rigaya daga Ubangijinka ba, (dajinkirin sakamako izuwa ranar Alƙiyama,) da an hukunci tsakanin mutane (a duniya) cikin abinda suke saɓawa a cikinsa (daga addini,) ayi wa kafirai azaba).

(ƘIRƘIRAR MUSHIRIKAI AYOYI)

20. Mutanen Makka suna cewa donme ba a saukar da aya gareshi daga Ubangijinsa ba, (tamfar daya kasance ga Annabawa, taguwa da sanda da hannu,) cene (dasu) "Sanin gaibu dai na ga Allah shi kaɗai, ni ida aike ne kaɗai a gareni, ku saurari azaba in baku bada gaskiya ba, haƙiƙa ni ina cikin masu sauraro tareda ku.

(DABI'AR MUTUM TA BUTULCEWA NI'IMAR ALLAH)

وَإِذَآ أَذَقْنَا ٱلنَّاسَ رَحْمَةً مِّنۢ بَعْدِ ضَرَّآءَ مَسَّتْهُمْ إِذَا لَهُم
مَّكْرٌ فِىٓ ءَايَاتِنَا ۚ قُلِ ٱللَّهُ أَسْرَعُ مَكْرًا ۚ إِنَّ رُسُلَنَا يَكْتُبُونَ
مَا تَمْكُرُونَ ﴿21﴾ هُوَ ٱلَّذِى يُسَيِّرُكُمْ فِى ٱلْبَرِّ وَٱلْبَحْرِ ۖ حَتَّىٰٓ إِذَا كُنتُمْ
فِى ٱلْفُلْكِ وَجَرَيْنَ بِهِم بِرِيحٍ طَيِّبَةٍ وَفَرِحُوا۟ بِهَا جَآءَتْهَا رِيحٌ
عَاصِفٌ وَجَآءَهُمُ ٱلْمَوْجُ مِن كُلِّ مَكَانٍ وَظَنُّوٓا۟ أَنَّهُمْ
أُحِيطَ بِهِمْ ۙ دَعَوُا۟ ٱللَّهَ مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ لَئِنْ أَنجَيْتَنَا مِنْ
هَٰذِهِۦ لَنَكُونَنَّ مِنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ﴿22﴾ فَلَمَّآ أَنجَىٰهُمْ إِذَا هُمْ يَبْغُونَ
فِى ٱلْأَرْضِ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ ۗ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّمَا بَغْيُكُمْ عَلَىٰٓ أَنفُسِكُم ۖ مَّتَٰعَ
ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ۖ ثُمَّ إِلَيْنَا مَرْجِعُكُمْ فَنُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿23﴾
إِنَّمَا مَثَلُ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا كَمَآءٍ أَنزَلْنَٰهُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَٱخْتَلَطَ بِهِۦ نَبَاتُ
ٱلْأَرْضِ مِمَّا يَأْكُلُ ٱلنَّاسُ وَٱلْأَنْعَٰمُ حَتَّىٰٓ إِذَآ أَخَذَتِ ٱلْأَرْضُ
زُخْرُفَهَا وَٱزَّيَّنَتْ وَظَنَّ أَهْلُهَآ أَنَّهُمْ قَٰدِرُونَ عَلَيْهَآ
أَتَىٰهَآ أَمْرُنَا لَيْلًا أَوْ نَهَارًا فَجَعَلْنَٰهَا حَصِيدًا كَأَن لَّمْ تَغْنَ بِٱلْأَمْسِ ۚ
كَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلْءَايَٰتِ لِقَوْمٍ يَتَفَكَّرُونَ ﴿24﴾ وَٱللَّهُ يَدْعُوٓا۟
إِلَىٰ دَارِ ٱلسَّلَٰمِ وَيَهْدِى مَن يَشَآءُ إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿25﴾

21. Idan muka ɗanɗanawa mutane rahama, (ruwa dayalwa,) bayan tsanani, (fari da wahala) daya same su, sai gasu suna ta makirci a cikin ayoyinmu (izgili da ƙaryatawa,) cene (dasu) "Allah ne mafi gaggawar sakamakon makirci, haƙiƙa jakadunmu masu kiyayewa suna rubuta makircin nan naku".

22. Shine wanda yake tafiyar daku ,a cikin sarari da kogi, har Lokacin da kuka kasance a cikin jirage, suka gudana daku ,da iska Lallausa, sukayi farin ciki da ita, sai iska mai karfi ta zo, kumfa kuma saitazo musu daga kowane wuri, kuma saisu tabbata haƙiƙa su an halakar dasu, to, saisu kira Allah suna masu tsarkakewar kira a gareshi Wallahi idan ka tserar da mu daga waɗannan tsarmakatai lalle zamu kasance masu godiyagareka da kaɗaitaka.

23. Yayin daya tserar dasu sai gasu suna zalunci a cikin ƙasa bada gaskiya ba, Yaku mutane zaluncin nan naku a kanku yake kawai! Shi dan amfanin rayuwar duniya ne kankani, sannan izuwa garemu makomar ku take mu baku labari da abinda kuka kasance kuna aikatawa.

(ISASSHEN MISALI NA RAYUWAR DUNIYA)

24. Haƙiƙa dahir dai misalin rayuwar duniya kamar ruwa ne da muka saukar dashi daga sama, tsirrran ƙasa suka cudanya saboda shi na daga abinda mutane suke ci, (alƙama, sha'ir da waninsu,) da dabbobi, har Lokacin da ƙasa ta riƙi adonta (na tsirrai,) tayi kwalliya, mutanen ta suka zaci cewa su haƙiƙa masu iko ne a kanta (na wajen cin moronta,) to, al'amarinmu sai yazo mata, (na azaba) da dare ko da rana, sai mu maida ita gir-babbiya kamar bata taɓazama ajiya ba, tamfar da muka rarrabe sanya wannan misali muke rarrabe ayoyi filla - filla ga mutane dasuke yin tunani.

KWADAITAR DA MUTANE SHIGA ALJANNA DA TSORATAR DASU SHIGA WUTA)

25. Allah yana kira izuwa gidan aminci, (aljanna) yana kira izuwa imani, yana shiriyar wanda yaga damar shiriyar dashi izuwa tafarki madaidaici.

(DARAJAR MUƘAMIN IHSANI DA UBA IZUWA ZATIN UBANGIJI MA-DAUKAKIN SARKI)

حزب

۞ لِّلَّذِينَ أَحْسَنُواْ ٱلْحُسْنَىٰ وَزِيَادَةٌ وَلَا يَرْهَقُ وُجُوهَهُمْ قَتَرٌ
وَلَا ذِلَّةٌ أُوْلَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَنَّةِ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿26﴾ وَٱلَّذِينَ
كَسَبُواْ ٱلسَّيِّـَٔاتِ جَزَآءُ سَيِّئَةِۭ بِمِثْلِهَا وَتَرْهَقُهُمْ ذِلَّةٌ
مَّا لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ مِنْ عَاصِمٍ كَأَنَّمَآ أُغْشِيَتْ وُجُوهُهُمْ
قِطَعًا مِّنَ ٱلَّيْلِ مُظْلِمًا أُوْلَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿27﴾
وَيَوْمَ نَحْشُرُهُمْ جَمِيعًا ثُمَّ نَقُولُ لِلَّذِينَ أَشْرَكُواْ مَكَانَكُمْ أَنتُمْ
وَشُرَكَآؤُكُمْ فَزَيَّلْنَا بَيْنَهُمْ وَقَالَ شُرَكَآؤُهُم مَّا كُنتُمْ إِيَّانَا
تَعْبُدُونَ ﴿28﴾ فَكَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدًا بَيْنَنَا وَبَيْنَكُمْ إِن كُنَّا
عَنْ عِبَادَتِكُمْ لَغَٰفِلِينَ ﴿29﴾ هُنَالِكَ تَبْلُواْ كُلُّ نَفْسٍ مَّآ أَسْلَفَتْ
وَرُدُّوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ مَوْلَىٰهُمُ ٱلْحَقِّ وَضَلَّ عَنْهُم مَّا كَانُواْ يَفْتَرُونَ ﴿30﴾
قُلْ مَن يَرْزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ أَمَّن يَمْلِكُ ٱلسَّمْعَ وَٱلْأَبْصَٰرَ
وَمَن يُخْرِجُ ٱلْحَيَّ مِنَ ٱلْمَيِّتِ وَيُخْرِجُ ٱلْمَيِّتَ مِنَ ٱلْحَيِّ وَمَن يُدَبِّرُ
ٱلْأَمْرَ فَسَيَقُولُونَ ٱللَّهُ فَقُلْ أَفَلَا تَتَّقُونَ ﴿31﴾ فَذَٰلِكُمُ
ٱللَّهُ رَبُّكُمُ ٱلْحَقُّ فَمَاذَا بَعْدَ ٱلْحَقِّ إِلَّا ٱلضَّلَٰلُ فَأَنَّىٰ تُصْرَفُونَ ﴿32﴾
كَذَٰلِكَ حَقَّتْ كَلِمَتُ رَبِّكَ عَلَى ٱلَّذِينَ فَسَقُوٓاْ أَنَّهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿33﴾

26. Shiga Aljanna da duba izuwa Zatin Allah sun tabbata ga wađanda suka tsoraci Allah a maƙamin ihsani, duhu ko wulakanci bazai rufe ƙuskokinsu ba, wađancananka sune yan aljanna, su madauwama ne a cikinta, (Allah ya sa mu cikinsu Amin).
27. Wađanda suka aikata miyagun ayyuka sakamakon mummunan aiki ya tabbata mummunan aiki kamarsa wulakanci na Lulluɓe ƙuskokinsu, basu da mai hana musu azabar Allah, kai kace an Lulluɓawa ƙuskokinsu dayanke yanke na dare mai duhu, wađancananka sune "yan wuta, su madauwama ne a cikinta.

(MATSAYI DAGA MATSAYAN RANAR ALƘIYAMA) :

28. Ambaci ranar da muke tare halitta bakiđaya, sannan mu fađa ga wađannan da sukayi shirka, ku Lazumci inda kuke, kuda abokan tarayyarku (gumaka,) to, muka rabe tsakaninsu da tsakanin muminai, abokan tarayyar tasu sukace (dasu) "Baku kasance mu kuke bautawa ba.
29. "To, Allah ya isa shaida tsakaninmu da ku, haƙiƙa mun kasance marabkana ga buran bautarku".
30. Wancanaiika rana ce, kowace kai zata đanđana abindata gabatar (na kuđarta,) za a mai dasu izuwa Allah majiɓincmsu tabbatacce, abinda suke ƙirƙira zai faku ga buransu.

(TABBATAR DA DAYANTAKAR ALLAH DA BATA SHIRKA, AKWAI RADDI CIKINSA GA SHUWU'IYA DA AIKHALIƘIYA)

31. Cene (dasu) wa yake azurta ku daga sama (da ruwa,) wa yake azurta ku daga ƙasa (da tsiri,) ko kuwa yake mallakar kunnuwa da idanuwa, (wato wa ya halittar muku su) wa yafitar da rayayye daga matacce, wa yafitar da matacce daga rayayye, wanene yake shirya al' amarin talikai? Da sannu zasu ce dakai Allah ne, to, cene donme ba kwa bada gaskiya.
32. To, wancananku (wanda ya aikata wađannan ayyuka) shine Allah Ubangijinku tabbatacce, to, wane abu ne bayan gaskiya, sai ɓata, (wato wanda yakuskure gaskiya, wato ibadar Allah ya tsinduma a cikin kogin bata ya halaka) to, donme ake juyar daku ,(ga buran imani tareda tsayawar hujja?)
33. Tamfar dayajuyar da wađannan ga buran imani hakana kalmar Ubangijinka ta tabbata a bisa wađanda suka kangarewa Allah, (iTace Lalle zan cika jahannama har ƙarshen ayar,) haƙiƙa su bazasu bada gaskiya ba.

قُلْ هَلْ مِن شُرَكَآئِكُم مَّنْ يَّبْدَؤُا الْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ قُلِ اللَّهُ
يَبْدَؤُا الْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ فَأَنّ۪يٰ تُوفَكُونَ ﴿34﴾ قُلْ هَلْ مِن شُرَكَآئِكُم
مَّنْ يَّهْدِے إِلَى الْحَقِّ قُلِ اللَّهُ يَهْدِے لِلْحَقِّ أَفَمَنْ يَّهْدِے إِلَى
الْحَقِّ أَحَقُّ أَنْ يُّتَّبَعَ أَمَّنْ لَّا يَهْدِے إِلَّا أَنْ يُّهْدَيٰ فَمَا لَكُمْ
كَيْفَ تَحْكُمُونَ ﴿35﴾ وَمَا يَتَّبِعُ أَكْثَرُهُمُۥ إِلَّا ظَنًّا إِنَّ الظَّنَّ
لَا يُغْنِے مِنَ الْحَقِّ شَيْـًٔا إِنَّ اللَّهَ عَلِيمٌۢ بِمَا يَفْعَلُونَ ﴿36﴾ * وَمَا كَانَ
هَٰذَا الْقُرْءَانُ أَنْ يُّفْتَرَيٰ مِن دُونِ اللَّهِ وَلَٰكِن تَصْدِيقَ
الَّذِے بَيْنَ يَدَيْهِ وَتَفْصِيلَ الْكِتَٰبِ لَا رَيْبَ فِيهِ مِن رَّبِّ الْعَٰلَمِينَ ﴿37﴾
أَمْ يَقُولُونَ افْتَرَيٰهُ قُلْ فَأْتُوا بِسُورَةٍ مِّثْلِهِۦ وَادْعُوا مَنِ اسْتَطَعْتُم
مِّن دُونِ اللَّهِ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿38﴾ بَلْ كَذَّبُوا بِمَا لَمْ يُحِيطُوا بِعِلْمِهِۦ
وَلَمَّا يَأْتِهِمْ تَأْوِيلُهُۥ كَذَٰلِكَ كَذَّبَ الَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ فَانظُرْ كَيْفَ كَانَ
عَٰقِبَةُ الظَّٰلِمِينَ ﴿39﴾ وَمِنْهُم مَّنْ يُّؤْمِنُ بِهِۦ وَمِنْهُم مَّن لَّا يُؤْمِنُ بِهِۦ
وَرَبُّكَ أَعْلَمُ بِالْمُفْسِدِينَ ﴿40﴾ وَإِن كَذَّبُوكَ فَقُل لِّے عَمَلِے وَلَكُمْ عَمَلُكُمْ
أَنتُم بَرِيٓـُٔونَ مِمَّا أَعْمَلُ وَأَنَا بَرِےٓءٌ مِّمَّا تَعْمَلُونَ ﴿41﴾ وَمِنْهُم مَّن
يَسْتَمِعُونَ إِلَيْكَ أَفَأَنتَ تُسْمِعُ الصُّمَّ وَلَوْ كَانُوا لَا يَعْقِلُونَ ﴿42﴾

ثمن

(TABBATAR DA TASHIN ALƘIYAMA DA MANA KI BISA KAFIRCI)

34. Cene, "Akwai daga abeban tarayyar ku wanda yake ƙagan halitta sannan ya karɓi ransa, sannan ya tasheshi (bayan ya mutu)". Cene, "Allah shine mai ƙagen halitta daga rashi sannan ya tasheshi (bayan ya mutu,) to, donme ake juyar daku ,(ga buran bautarsa tareda tsayawar dalili?)"

35. Cene, "Akwai daga ababen tarayyar ku wanda yake shiryarwa izuwa gaskiya, (da kafa hujjoji ta halittar hujjoji a zuci). Cene Allah ne yake shiriya izuwa gaskiya, shin, to, wanda yake shiriya izuwa gaskiya (wato Allah,) shi yafi cancanta a bi shi, ko wanda baya shiryarwa sai dai a shirye shi. Me ya same ku ne, ƙaƙa kuke wannan kukunci (ɓatacce na bin wanda bai kamata a bi shi ba).

36. Yawaicinsu basa bi (a cikin bautar gumaka) sai zato, (Don sun ,a kwaikwayon iyayensune kawai,) haƙiƙa zato baya wadatar da komai na daga wajen gaskiya, haƙiƙa Ubangiji masanine da abinda suke aikatawa.

(ALƘUR' ANI ZANCEN ALLAH NE, MU UJIZA NE KUMA GA MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

37. Wannan Alƙur' ani bai kasance a ƙirƙire shi daga wanin Allah ba, sai dai an saukar dashine don gasgata abinda yake gabansa (na daga littattafai) da rarrabe abinda Allah ya hukunta (na hukunce - hukunce da waninsa,) ba kokwanto a cikinsa, daga Ubangijin talikai yake.

38. Haba! ko suna cewa, "Ya ƙirƙire shine?" to, cene, "To, kuzo dasura guda ɗaya misalinsa (a cikin fasaha da balaga, a bisa fuskar ƙirƙira domin ku Larabawa ne fasihai kama ta,) ku kirawo wanda kuka sami iko ba Allah ba (ya taimake ku,) in kun kasance magasgata (a cikin cewa ƙirƙira ne". Basu sami iko kan wannan ba sai Allah yace);

39. Kai dai sun ƙaryatada abinda basu kewaye da ilimi dashi ba ne, (Alƙur'ani) har yau aƙibar abinda yake cikinsa (na daga narko) bai zo musu ba, kamar wancananka ƙaryatawa,waɗanda suke gabansu suka ƙaryata (manzanni,) kai duba ƙaƙa ƙarshen azzalumai ya kasance, (da ƙaryata manzanni sun halaka, hakana zamu halakar da waɗannan).

(MATSAYIN MUSHIRIKAI DAGA ALƘUR'ANI DA MATSAYIN ANNABI A GARESU, SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

40. (Alƙur'ani) akwai daga garesu wanda bazai bada gaskiya dashi ba (har abada,) Ubangijinka ne masani da masu ɓarna, (barazana ce ga kafirai).

41. In sun ƙaryata ka, to, cene (dasu) "Aikina yana gareni, aikinku yana gareku, (kowa zai gamu da sakamakon aikinsa,) ku makubuta ne daga abinda nake aikatawa, ni makubuci ne daga abinda kuke aikatawa (wannan shafaffe ne da ayar kansakali).

42. Akwai daga cikinsu waɗanda suke sauraro izuwa gareka (idan kana karatun Alƙur'ani,) shin, to, kai, ka jiyar da kurama, kodasun kasance basu da hankali (tareda kumntarsu wato su kamar kurame suke a cikin rashin amfani da abinda ake karanta musu).

وَمِنْهُم مَّن يَنظُرُ إِلَيْكَ أَفَأَنتَ تَهْدِي الْعُمْيَ وَلَوْ كَانُوا
لَا يُبْصِرُونَ ﴿43﴾ إِنَّ اللَّهَ لَا يَظْلِمُ النَّاسَ شَيْئًا وَلَٰكِنَّ النَّاسَ
أَنفُسَهُمْ يَظْلِمُونَ ﴿44﴾ وَيَوْمَ يَحْشُرُهُمْ كَأَن لَّمْ يَلْبَثُوا إِلَّا سَاعَةً
مِّنَ النَّهَارِ يَتَعَارَفُونَ بَيْنَهُمْ قَدْ خَسِرَ الَّذِينَ كَذَّبُوا بِلِقَاءِ اللَّهِ
وَمَا كَانُوا مُهْتَدِينَ ﴿45﴾ وَإِمَّا نُرِيَنَّكَ بَعْضَ الَّذِي نَعِدُهُمْ أَوْ نَتَوَفَّيَنَّكَ
فَإِلَيْنَا مَرْجِعُهُمْ ثُمَّ اللَّهُ شَهِيدٌ عَلَىٰ مَا يَفْعَلُونَ ﴿46﴾ وَلِكُلِّ
أُمَّةٍ رَّسُولٌ فَإِذَا جَاءَ رَسُولُهُمْ قُضِيَ بَيْنَهُم بِالْقِسْطِ وَهُمْ
لَا يُظْلَمُونَ ﴿47﴾ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا الْوَعْدُ إِن كُنتُمْ صَادِقِينَ ﴿48﴾
* قُل لَّا أَمْلِكُ لِنَفْسِي ضَرًّا وَلَا نَفْعًا إِلَّا مَا شَاءَ اللَّهُ
لِكُلِّ أُمَّةٍ أَجَلٌ إِذَا جَاءَ أَجَلُهُمْ فَلَا يَسْتَأْخِرُونَ سَاعَةً
وَلَا يَسْتَقْدِمُونَ ﴿49﴾ قُلْ أَرَأَيْتُمْ إِنْ أَتَاكُمْ عَذَابُهُ بَيَاتًا أَوْ نَهَارًا
مَّاذَا يَسْتَعْجِلُ مِنْهُ الْمُجْرِمُونَ ﴿50﴾ أَثُمَّ إِذَا مَا وَقَعَ آمَنتُم بِهِ
آلْآنَ وَقَدْ كُنتُم بِهِ تَسْتَعْجِلُونَ ﴿51﴾ ثُمَّ قِيلَ لِلَّذِينَ ظَلَمُوا ذُوقُوا عَذَابَ
الْخُلْدِ هَلْ تُجْزَوْنَ إِلَّا بِمَا كُنتُمْ تَكْسِبُونَ ﴿52﴾ وَيَسْتَنبِئُونَكَ
أَحَقٌّ هُوَ قُلْ إِي وَرَبِّي إِنَّهُ لَحَقٌّ وَمَا أَنتُم بِمُعْجِزِينَ ﴿53﴾

ربع

43. Akwai daga cikinsu wanda yake duba izuwa gareka, shin, to, kai ka shiryi makafi kodasun kasance basa gani? (An kwatanta su da makafi a cikin rashin shiriya, makantar zuci tafi makantar ido).
44, Haƙiƙa Ubangiji baya zaluntar kowa komai sai dai su mutane ne dai suke zaluntar kawukansu.

(UNIYABA MATABBACI CE BA)

45. Ambaci ranar da muke tara su kai ka .ce basu zauna (a ƙaburbura ba) sai sa'a kaɗan ta rana, suna sanayya tsakaninsu, (ba' alinsu yana sanin ba'ali yayin da aka tashe su daga ƙabari, sannan sanayyar ta yanke saboda tsananin tsarmakatai,) haƙiƙa waɗanda suka ƙaryatada tashin alƙiyama sun taɓe, basu kasance shiryayyu ba.

(RADDI KAN MUSHIRIKAI DA KUMA GAGGAWARSU DA SAUKAR AZABA)

46. In mun nuna maka ba' alin abinda muke musu alwashi dashi na azaba (a cikin rayuka to, shi ke nan,) ko muka karɓe ka gaban bamu azabce su ba, to, izuwa garemune makomarsu, sannan Allah shine mai ganin abinda suke aikatawa (na daga ƙaryatawa da kafircewa zai ɗanɗana musu mummunar azaba).
47. Kowace al'umma (daga al'ummai) suna da jakada, idan manzansu yazo musu suka ƙaryata shi, sai mu yi hukunci tsakaninsu da adalci, (mu yi musu azaba, mu tserar da manzon tareda waɗanda suka gasgata shi). Su ba a zaluntarsu, (ayi musu azaba bada laifi ba, hakana zamu aikatada waɗannan.)
48. Suna cewa, "Yaushe ne wannan alKawari (na azaba) inkun kasance magasgata (a cikinsa)".
49. Cene, "Ni ban mallaki cuta ko amfani ga kaina ba, sai abinda Allah ya nufa (ya bani iko a kansa, yaya zan mallakiyi muku azaba,) kowace al' umma tana da mudda (abar sani ga halakar ta,) idan ajalinsu (na halaka) yazo, to, baza ayi musujinkiri ga buransa ba sa'a daya baza a gaggautar dasu a kansa ba".
50. Cene, "Ku bamu labari in azabar Allah tazo mukuda dare ko da rana, meye mushirikai suke gaggawa daga gareshi (na azaba?)"
51. To, kuma idan ya auku a garekune zaku bada gaskiya da Ubangiji? Baza a karɓi ban gaskiyarku ba, (za a ce da ku,) "Sai yanzu kuka bada gaskiya, alhali kun kasance kuna garajen saukarsa (don izgili)".
52. Sannan za a faɗa ga waɗanda suka zalunci kansu, "Ku ɗanɗani azabar dauwama, ba a saka muku sai abinda kuka kasance kuka aikata".
53. Suna neman ka basu Labari, shin gaskiya ne shi azabar nan? Cene (dasu,) "I, na' am na rantse da Ubangijina haƙiƙa shi Lalle gaskiya ne, ku ba masu tserewa azabane ba".

وَلَوْ أَنَّ لِكُلِّ نَفْسٍ ظَلَمَتْ مَا فِي الْأَرْضِ لَافْتَدَتْ بِهِۦ
وَأَسَرُّوا۟ النَّدَامَةَ لَمَّا رَأَوُا۟ الْعَذَابَ وَقُضِيَ بَيْنَهُم بِالْقِسْطِ
وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿54﴾ أَلَا إِنَّ لِلَّهِ مَا فِي السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ
أَلَا إِنَّ وَعْدَ اللَّهِ حَقٌّ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿55﴾ هُوَ يُحْيِۦ
وَيُمِيتُ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿56﴾ يَا أَيُّهَا النَّاسُ قَدْ جَاءَتْكُم مَّوْعِظَةٌ
مِّن رَّبِّكُمْ وَشِفَاءٌ لِّمَا فِي الصُّدُورِ وَهُدًى وَرَحْمَةٌ لِّلْمُؤْمِنِينَ ﴿57﴾
قُلْ بِفَضْلِ اللَّهِ وَبِرَحْمَتِهِۦ فَبِذَٰلِكَ فَلْيَفْرَحُوا۟ هُوَ خَيْرٌ مِّمَّا يَجْمَعُونَ ﴿58﴾
قُلْ أَرَأَيْتُم مَّا أَنزَلَ اللَّهُ لَكُم مِّن رِّزْقٍ فَجَعَلْتُم مِّنْهُ
حَرَامًا وَحَلَٰلًا قُلْ ءَآللَّهُ أَذِنَ لَكُمْ أَمْ عَلَى اللَّهِ
تَفْتَرُونَ ﴿59﴾ وَمَا ظَنُّ الَّذِينَ يَفْتَرُونَ عَلَى اللَّهِ الْكَذِبَ
يَوْمَ الْقِيَٰمَةِ إِنَّ اللَّهَ لَذُو فَضْلٍ عَلَى النَّاسِ وَلَٰكِنَّ
أَكْثَرَهُمْ لَا يَشْكُرُونَ ﴿60﴾ * وَمَا تَكُونُ فِي شَأْنٍ وَمَا تَتْلُوا۟ مِنْهُ
مِن قُرْءَانٍ وَلَا تَعْمَلُونَ مِنْ عَمَلٍ إِلَّا كُنَّا عَلَيْكُمْ شُهُودًا إِذْ تُفِيضُونَ
فِيهِ وَمَا يَعْزُبُ عَن رَّبِّكَ مِن مِّثْقَالِ ذَرَّةٍ فِي الْأَرْضِ
وَلَا فِي السَّمَاءِ وَلَا أَصْغَرَ مِن ذَٰلِكَ وَلَا أَكْبَرَ إِلَّا فِي كِتَٰبٍ مُّبِينٍ ﴿61﴾

ثمن

54. Da cewa duk abinda yake cikin ƙasa yana ga kowace kai da tayi kafirci, da saitayi fansa dashi daga azabar Allah ranar Lahira, sun bayyana! nadama yay-in da suka ga azaba, ƙarara! An - yi hukunci tsakaninsu da adalci, su baza a zalunce su (komai ba).
55. To, jama'a haƙiƙa abinda yake sammai da ƙassai duk na Allah ne, to, jama'a haƙiƙa alƙawarin Allah (da tashin alƙiyama da sakamako) gaskiya ne, sai dai yawaicin mutane basu san haka ba!
56. Shine mai rayawa mai kashewa, izuwa gareshi za a koma da ku.

(ALƘUR'ANI DA AMFANINSA)

57. Yaku mutane! Haƙiƙa gargadi yazo muku daga Ubangijinku, (shine alƙur'ani.) da waraka ga abinda yake cikin ƙiraza, (na daga munanan miyagun ƙudire -ƙudire da kokwanto,) dashiriya daga bata, da jinƙai ga muminai (dashi Alƙur' ani).
58. Faɗa musu "Kuyi farin ciki da falalar Allah, (Musulunci,) da rahama tasa alƙur' ani, to, da wancananka zakuyi farin cikin kawai, shi yafi alheri daga abinda kuke tattarawa (na duniya).

(BANDA ALLAH BA MAI IALATTAWA KO HARAMTAWA)

59, Cene, "Ku bani Labarin abinda Allah ya halitta a gareku na ar-ziki, kuka sanya haram daga gareshi da halal (kamar Bahira da Sa'ibada dokokin zamani waɗanda basu dace da Alƙur' ani ba). Cene shin Allah ne yayi muku izini a cikin wannan? (A'a!) haka ku dai kuna kuta ƙarya ne ga Allah.
60. Meye zaton waɗanda suke girba ƙarya ne ga Ubangiji ranar alƙiyama! (Suna zaton bazaiyi musu uƙuba ba ne? Kai! uƙuba zaiyi musu,) haƙiƙa Ubangiji ma'abucin falala ne a bisa mutane, (da jinkirta musu da ni' imtasu,) sai dai yawaicinsu basa godewa Allah.

(LA'AKARIN ALLAH DA BAYINSA DA KEWAYEWARSA KOWANE ABU DA ILIMINSA)

61. Baka kasance (Ya Muhammadu Sallallahu alaika wasallama) a cikin sha'ani ba, ko karanta wani daga alƙur'ani da aka saukar gareka, koku aikata wani abu na aiki (ya al'ummar Annabi Sallallahu alaihi wasallama, face mun kasance masu la'akari a kanku, (muna kallon ku, ƙwar) zamanin da kuke kutsawa a cikinsa, babu abinda yake buyaga buran Ubangijinka na daga awon zarra, (kuma ko kurar taga, ko kwayar iska,) a cikin ƙasa ko a cikin sama, wala mafi ƙanƙanta daga wancananka, (shine Jauharul --fardu) wala mafi girma daga wancananka, face yana cikin Littafi mabayyani, (shine Lauhul - Mahafuzu).

أَلَآ إِنَّ أَوْلِيَآءَ ٱللَّهِ لَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿62﴾
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَكَانُوا۟ يَتَّقُونَ ﴿63﴾ لَهُمُ ٱلْبُشْرَىٰ فِى ٱلْحَيَوٰةِ
ٱلدُّنْيَا وَفِى ٱلْءَاخِرَةِ ۚ لَا تَبْدِيلَ لِكَلِمَٰتِ ٱللَّهِ ۚ
ذَٰلِكَ هُوَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿64﴾ وَلَا يَحْزُنكَ قَوْلُهُمْ ۘ
إِنَّ ٱلْعِزَّةَ لِلَّهِ جَمِيعًا ۚ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْعَلِيمُ ﴿65﴾ أَلَآ إِنَّ لِلَّهِ
مَن فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِى ٱلْأَرْضِ ۗ وَمَا يَتَّبِعُ ٱلَّذِينَ
يَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ شُرَكَآءَ ۚ إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّ
وَإِنْ هُمْ إِلَّا يَخْرُصُونَ ﴿66﴾ هُوَ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ
ٱلَّيْلَ لِتَسْكُنُوا۟ فِيهِ وَٱلنَّهَارَ مُبْصِرًا ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ
لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَسْمَعُونَ ﴿67﴾ قَالُوا۟ ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ وَلَدًا ۗ
سُبْحَٰنَهُۥ ۖ هُوَ ٱلْغَنِىُّ ۖ لَهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۚ
إِنْ عِندَكُم مِّن سُلْطَٰنٍۭ بِهَٰذَآ ۚ أَتَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ
مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿68﴾ قُلْ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَفْتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ
ٱلْكَذِبَ لَا يُفْلِحُونَ ﴿69﴾ مَتَٰعٌ فِى ٱلدُّنْيَا ثُمَّ إِلَيْنَا مَرْجِعُهُمْ
ثُمَّ نُذِيقُهُمُ ٱلْعَذَابَ ٱلشَّدِيدَ بِمَا كَانُوا۟ يَكْفُرُونَ ﴿70﴾

(AULIYA' UL - LAHI)

62. To, jama'a! haƙiƙa Waliyyan Allah ba tsoro garesu baza suyi bakin ciki ba (a Lahira,).
63. Sune waɗanda suka bada gaskiya, suka kasance suna tsoron Allah.
64. Albishir ya tabbata garesu a rayuwar duniya, (mafarki nagari da karamomi, da biyan bukace -bukace cikin sauki; natijar istikama a duniya,) a lahira kuma (aljanna da abinda yake cikinta na daga ni 'imomi madauwama,) ba musanyawar alƙawarce alƙawarcen Ubangiji, wancananka shine rabo maigirma.

(BUWAYA TANA GA ALLAH MADAUKAKIN SARKI BAKI DAYA)

65. Kada faɗinsu ya baƙanta maka dasuke (cewa kai ba manzo ba ne,) haƙiƙa buwaya ta tabbata ga Allah bakiɗaya, yana bashe ta ga wanda yaga dama, shine maiji mai sani.
66. To, jama'a haƙiƙa abinda yake sammai da ƙassaina Allah ne, (mallaka da halittada bauta,) waɗanda suke bautawa wanin Allah (na daga gumaka,) basuna bin sharikai bane a haƙiƙa, a'a! Allah ya girma ga buran wannan, su suna bin zato ne kawai, zatonsu cewa ita iyayen giji ce ɗaza tacece su, su basu kasance ba sai maƙaryata.
67. Shine wanda yasanya muku dare domin ku nutsu a cikinsa, yasanya rana mai sa ku ga komai tangaran, haƙiƙa akwai ayoyi a cikin wancananka (masu nuna girman Allah da kadaitarsa,) ga mutane masu jin wa'azin alƙur'ani da lura.

(TSARKAKE ALLAH MADAUKAKIN SARKI WACCE TA KUNSHI TAWAKKULI DA ALLAH)

68. (Su Yahudu ɗa Nasara da masu cewa Mala'iku "ya"yan Allah ne,) sukace "Allah ya riƙi ɗa" Ubangiji yace (dasu) "Tsarki ya tabbata ga Allah ga buran ɗa, shine mawadaci (ga buran kowa,) abinda yake sammai da ƙassaina Allah ne (mallaka da halittada bauta,) bakuda wata hujja a garekuda wannan magana, donme kuke faɗan abinda baku sani ba game da Allah?
69. Cene, "Haƙiƙa waɗanda suke ƙirƙira ƙaryaga Allah (da dangana ɗa gareshi,) bazasu tsira ba".
70. Jin daɗi kaɗan (na garesu a duniya,) sannan izuwa garemu makomarsu da mutuwa, sannan mu ɗanɗana musu azaba mai tsanani (bayan mutuwa saboda zamansu kafirai).

ربع

* وَٱتْلُ عَلَيْهِمْ نَبَأَ نُوحٍ إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِۦ يَٰقَوْمِ إِن كَانَ كَبُرَ
عَلَيْكُم مَّقَامِى وَتَذْكِيرِى بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَعَلَى ٱللَّهِ تَوَكَّلْتُ
فَأَجْمِعُوٓاْ أَمْرَكُمْ وَشُرَكَآءَكُمْ ثُمَّ لَا يَكُنْ أَمْرُكُمْ
عَلَيْكُمْ غُمَّةً ثُمَّ ٱقْضُوٓاْ إِلَىَّ وَلَا تُنظِرُونِ ﴿71﴾ فَإِن تَوَلَّيْتُمْ
فَمَا سَأَلْتُكُم مِّنْ أَجْرٍ إِنْ أَجْرِىَ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِ وَأُمِرْتُ
أَنْ أَكُونَ مِنَ ٱلْمُسْلِمِينَ ﴿72﴾ فَكَذَّبُوهُ فَنَجَّيْنَٰهُ وَمَن مَّعَهُۥ
فِى ٱلْفُلْكِ وَجَعَلْنَٰهُمْ خَلَٰٓئِفَ وَأَغْرَقْنَا ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا
فَٱنظُرْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلْمُنذَرِينَ ﴿73﴾ ثُمَّ بَعَثْنَا مِنۢ بَعْدِهِۦ رُسُلًا
إِلَىٰ قَوْمِهِمْ فَجَآءُوهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ فَمَا كَانُواْ لِيُؤْمِنُواْ بِمَا كَذَّبُواْ بِهِۦ
مِن قَبْلُ كَذَٰلِكَ نَطْبَعُ عَلَىٰ قُلُوبِ ٱلْمُعْتَدِينَ ﴿74﴾ ثُمَّ بَعَثْنَا مِنۢ
بَعْدِهِم مُّوسَىٰ وَهَٰرُونَ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ وَمَلَإِيْهِۦ بِـَٔايَٰتِنَا فَٱسْتَكْبَرُواْ
وَكَانُواْ قَوْمًا مُّجْرِمِينَ ﴿75﴾ فَلَمَّا جَآءَهُمُ ٱلْحَقُّ مِنْ عِندِنَا قَالُوٓاْ
إِنَّ هَٰذَا لَسِحْرٌ مُّبِينٌ ﴿76﴾ قَالَ مُوسَىٰٓ أَتَقُولُونَ لِلْحَقِّ لَمَّا جَآءَكُمْ أَسِحْرٌ هَٰذَا
وَلَا يُفْلِحُ ٱلسَّٰحِرُونَ ﴿77﴾ قَالُوٓاْ أَجِئْتَنَا لِتَلْفِتَنَا عَمَّا وَجَدْنَا عَلَيْهِ ءَابَآءَنَا
وَتَكُونَ لَكُمَا ٱلْكِبْرِيَآءُ فِى ٱلْأَرْضِ وَمَا نَحْنُ لَكُمَا بِمُؤْمِنِينَ ﴿78﴾

(ƘISSAR ANNABI NUHU ALAIHISSALAM)

71. Karanta musu (Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama) babbar magana ta Annabi Nuhu (Alaihissalam) yayin daya faɗa ga mutanensa, "Yaku mutanena in zamana cikinku ya kasance wa-hala a garekuda gargaɗm da nake mukuda ayoyin Allah, to na dogara ga Allah shi kaɗai, to ku shirya al'amarinku (watau kuyi mini duk abinda zakuyi mini) tareda abokan tarayyarku, sannan kada al' amarinku ya zama ɓoyayye a gareku, (ku fito a fili da manufarku,) sannan ku zartar da abinda kuke nufin kuyi mini kar kuyi mini sauraro.

72. "To, in kun juya bayaga barin gargaɗina to ban tanbaye ku Lada bisa ida aike ba, Ladana bai kasance ba illa ga Allah, an umarce ni in kasance daga Musulmai.

73. To, suka ƙaryata shi, muka tserar dashi da waɗanda suke tare dashi a cikin jirgi, muka sanya Waɗanda suke tare dashi masu mayewa a cikin ƙasa, muka nutsar da waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu (da ruwan Dufana) Ka duba ƙaƙa ƙarshen ababen gargaɗarwa ya kasance? (Haka zamu aikatada waɗanda suka ƙaryata ka).

(ALLAH BAYA CANJA AL'ADARSA)

74. Sannan muka aiko Manzanni bayan Annabi Nuhu izuwa mutanensu, (kamar Annabi Ibrahim da Hudu da Salihu tsiran Allah ya tabbata garesu,) sukazo musu da mu'ujuzozi, basu kasance masu gasgatawa da abinda suka ƙaryata dashi ba, tun gaban aiko manzanni garesu, hakana muke yimƙewa a bisa zukatan masu shisshigi (bazata karɓi imani ba, kamar yadda muka yimƙe zukatan waɗancananƙa).

(ƘISSAR ANNABI MUSA TAREDA FIR' AUNA WACCE TA ƘUNSHI UBANGIJI BAYA GYARA AIKIN MABAR NATA. UBANGIJI MAITABBATAR DA GASKIYA NE -KO DA KAFURAI SUNƘI)

75. Sannan muka aiko Annabi Musa da Annabi Haruna, tsiran Allah ya tabbata a garesu bayansu izuwa Fir'auna da mutanensa da ayoyinmu (guda tara) sukayi girman kai ga buran imani da ita,) sun kasance mutane ma'abota Laifi.

76. Yayin da gaskiya tazo musu daga garemu sai Sukace, "Wannan Lalle tsafi ne mabayyani".

77. Sai Annabi Musa (tsiran Allah dayardar Allah ta tabbata a gareshi) yace, "Yanzu kwa dinga faɗa ga gaskiya yayin datazo muku cewa tsafi ce,yanzu wannan tsafi ne (gashi ko wanda yayi shiya tsira ya bata tsafin matsafa? A'a ba tsafi ba ne,) matsafa bazasu rabauta ba".

78. Sukace, "Kazo mana ne donka juyar da mu ga barin abinda muka samu iyayenmu a kansa bunƙasa a cikin kasar Misira ta tabbata a gareku, mu bazamu gasgataku ba".

وَقَالَ فِرْعَوْنُ ٱئْتُونِي بِكُلِّ سَٰحِرٍ عَلِيمٍ ﴿79﴾ فَلَمَّا جَآءَ ٱلسَّحَرَةُ
قَالَ لَهُم مُّوسَىٰٓ أَلْقُواْ مَآ أَنتُم مُّلْقُونَ ﴿80﴾ فَلَمَّآ أَلْقَوْاْ
قَالَ مُوسَىٰ مَا جِئْتُم بِهِ ٱلسِّحْرُ إِنَّ ٱللَّهَ سَيُبْطِلُهُۥٓ
إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُصْلِحُ عَمَلَ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿81﴾ وَيُحِقُّ ٱللَّهُ ٱلْحَقَّ بِكَلِمَٰتِهِۦ
وَلَوْ كَرِهَ ٱلْمُجْرِمُونَ ﴿82﴾ * فَمَآ ءَامَنَ لِمُوسَىٰٓ إِلَّا ذُرِّيَّةٌ مِّن قَوْمِهِۦ
عَلَىٰ خَوْفٍ مِّن فِرْعَوْنَ وَمَلَإِيْهِمْ أَن يَفْتِنَهُمْ وَإِنَّ فِرْعَوْنَ
لَعَالٍ فِي ٱلْأَرْضِ وَإِنَّهُۥ لَمِنَ ٱلْمُسْرِفِينَ ﴿83﴾ وَقَالَ مُوسَىٰ يَٰقَوْمِ
إِن كُنتُمْ ءَامَنتُم بِٱللَّهِ فَعَلَيْهِ تَوَكَّلُوٓاْ إِن كُنتُم مُّسْلِمِينَ ﴿84﴾
فَقَالُواْ عَلَى ٱللَّهِ تَوَكَّلْنَا رَبَّنَا لَا تَجْعَلْنَا فِتْنَةً لِّلْقَوْمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿85﴾
وَنَجِّنَا بِرَحْمَتِكَ مِنَ ٱلْقَوْمِ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿86﴾ وَأَوْحَيْنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰ
وَأَخِيهِ أَن تَبَوَّءَا لِقَوْمِكُمَا بِمِصْرَ بُيُوتًا وَٱجْعَلُواْ بُيُوتَكُمْ
قِبْلَةً وَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَبَشِّرِ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿87﴾ وَقَالَ مُوسَىٰ
رَبَّنَآ إِنَّكَ ءَاتَيْتَ فِرْعَوْنَ وَمَلَأَهُۥ زِينَةً وَأَمْوَٰلًا فِي ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا
رَبَّنَا لِيُضِلُّواْ عَن سَبِيلِكَ رَبَّنَا ٱطْمِسْ عَلَىٰٓ أَمْوَٰلِهِمْ وَٱشْدُدْ
عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ فَلَا يُؤْمِنُواْ حَتَّىٰ يَرَوُاْ ٱلْعَذَابَ ٱلْأَلِيمَ ﴿88﴾

ثمن

79. Sai fir'auna yace, "Kuzo mini da dukkan matsafi gwani a cikin tsafi".

80. Yayin da matsafa sukazo sai Annabi Musa (yardar Allah ta tabbata gareshi) yace (dasu bayan sunce dashi ko ka jefa ko mu jefa,) "Ku jefa abinda zakujefa".

81. Yayin da suka jefa igiyoyinsu da sandunansu sai Annabi Musa yace dasu, "Abindaku ,kazo dashin nan shine tsafi, haƙiƙa Allah zai ɓata shi, Lalle ALLAH baya gyara aikin maɓamata".

82. Allah yana tabbatar da gaskiya da kalmominsa (alƙawarorinsa) koda kafurai masu laifi basu yarda ba.

HA'ANIN ANNABI MUSA ALAIHISSALAM TAREDA MUTANENSA)

83. Ba wanda ya bada gaskiya da Annab.i Musa sai zuriyya daga "ya" yayen mutanen fir' auna , a bisa tsoro da Fir' auna da mutanensa, (don tsoron ya juyar dasu ga buran addininsa, yayi musu azaba,) haƙiƙa Fir' auna mai girman kaine a cikin kasar Misra, haƙiƙa Fir'auna lalle yana daga cikin masu ɓarna, masu da'awar Allantaka.

84. Annabi Musa (Alaihissalam) yace "Yaku mutanena in kun kasance kun bada gaskiya da Allah, to, ku dogara a kansa shi kaɗai in kun kasance Musulmai".

85. Sukace, "Mun dogara ga Allah shi kaɗai, Ya Ubangijinmu kadaka sanya mu fitina a bisa mutane kafirai, (kadaka basu rinjaye su zaci su a kan gaskiya suke).

86. "Ka tserar da mu da jinkanka daga mutane kafirai".

87. Muka aiko izuwa Annabi Musa da dan uwansa Annabi Haruna (Alaihimassalam) cewa ku riƙi gidaddaji ga mutanenku a Misra, ku sanya ɗakunanku gurin salla, (kuyi salla a ciki, domin ku amince daga tsoro, alhali Fir'auna ya hana su salla,) Ku cika salla, kayi wa muminai albishir da aljanna".

(MUMMUNAR ADDU'AR ANNABI MUSA ALAIHISSALAM A KAN FIR'AUNA DA MUTANENTSA)

88. Annabi musa (Alaihissalam) yace, "haƙiƙa ka baiwa Fir' auna da mutanensa kayan ado da dukiyoyi a cikin rayuwar duniya, ya Ubangijinmu, ka basu wannan ne don ƙarshen abin su ɓatar ga buran addininka, ya Ubangijinmu yimƙe a bisa dukiyoyinsu (ka shafe ta) ko ɗaure a kan zukatansu, kadasu bada gaskiya sai sun ga azaba mai raɗaɗi," (yayi musu mugunyar addu'a, Annabi Haruna yace amin a kanta).

ربع

قَالَ قَدُ اُجِيبَت دَّعْوَتُكُمَا فَاسْتَقِيمَا وَلَا تَتَّبِعَآنِّ سَبِيلَ
اَ۬لذِينَ لَا يَعْلَمُونَ ﴿89﴾ وَجَٰوَزْنَا بِبَنِےٓ إِسْرَآءِيلَ اَ۬لْبَحْرَ فَأَتْبَعَهُمْ
فِرْعَوْنُ وَجُنُودُهُۥ بَغْياٗ وَعَدْواً حَتَّيٰٓ إِذَآ أَدْرَكَهُ اُ۬لْغَرَقُ
قَالَ ءَامَنتُ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا اَ۬لذِےٓ ءَامَنَتْ بِهِۦ بَنُوٓاْ إِسْرَآءِيلَ
وَأَنَا مِنَ اَ۬لْمُسْلِمِينَ ﴿90﴾ ءَآلَٰنَ وَقَدْ عَصَيْتَ قَبْلُ وَكُنتَ مِنَ
اَ۬لْمُفْسِدِينَ ﴿91﴾ فَالْيَوْمَ نُنَجِّيكَ بِبَدَنِكَ لِتَكُونَ لِمَنْ خَلْفَكَ ءَايَةٗ
وَإِنَّ كَثِيراٗ مِّنَ اَ۬لنَّاسِ عَنْ ءَايَٰتِنَا لَغَٰفِلُونَ ﴿92﴾ * وَلَقَدْ بَوَّأْنَا
بَنِےٓ إِسْرَآءِيلَ مُبَوَّأَ صِدْقٖ وَرَزَقْنَٰهُم مِّنَ اَ۬لطَّيِّبَٰتِ فَمَا اَ۪خْتَلَفُواْ
حَتَّيٰ جَآءَهُمُ اُ۬لْعِلْمُ إِنَّ رَبَّكَ يَقْضِے بَيْنَهُمْ يَوْمَ اَ۬لْقِيَٰمَةِ فِيمَا
كَانُواْ فِيهِ يَخْتَلِفُونَ ﴿93﴾ فَإِن كُنتَ فِے شَكّٖ مِّمَّآ أَنزَلْنَآ إِلَيْكَ
فَسْـَٔلِ اِ۬لذِينَ يَقْرَءُونَ اَ۬لْكِتَٰبَ مِن قَبْلِكَ لَقَدْ
جَآءَكَ اَ۬لْحَقُّ مِن رَّبِّكَ فَلَا تَكُونَنَّ مِنَ اَ۬لْمُمْتَرِينَ ﴿94﴾
وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ اَ۬لذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِ اِ۬للَّهِ فَتَكُونَ مِنَ
اَ۬لْخَٰسِرِينَ ﴿95﴾ إِنَّ اَ۬لذِينَ حَقَّتْ عَلَيْهِمْ كَلِمَٰتُ رَبِّكَ لَا يُومِنُونَ ﴿96﴾
وَلَوْ جَآءَتْهُمْ كُلُّ ءَايَةٍ حَتَّيٰ يَرَوُاْ اُ۬لْعَذَابَ اَ۬لْأَلِيمَ ﴿97﴾

89. Ubangiji yace, "Haƙiƙa an amsa addu'arku, (aka shafe dukiyoyinsu suka koma duwarwatsu, Fir;auna bai bada gaskiyaba har saida nitsewa ta riske shi,) to Kuyi ƙyama kan aike da kira har izuwa azabatazo musu, kadaku ,daka ta waɗanda basu san (gaskiyaba a cikin gaggawarsu, ƙaddara ta Ance ya zauna bayanta shekara arba' in).

(TSIRAN BANI - ISRA'ILA DA NUTSEWAR FIR' AUNA)

90. Muka ƙetare kogi da Bani -Isra'ila, to Fir 'auna ya riske su da rundinarsa don zalunci dashisshigi har dai Lokacin da nutsewa ta riske shi, sai yace "Ni na bada gaskiya da wanda Bani - Isra'ila suka bada gaskiya dashi, ni ina daga cikin Musulmi," (ya maimaita don a karɓa daga gareshi, to, ba a karɓa ba, sai Mala'ika Jibrilu ya afa tabo a bakinsa na daga kogi don tsoron kada rahama ta same shi).

91. To, a yanzu ne zaka bada gaskiya? Alhali ka ƙi bada gaskiya tun gaba, ka kasance daga cikin mabarnata!

92. To, a yau muna tserar dakai daga cikin kogi da jikinka (wanda ba rai,) donka zama izina ga wanda yake baynaka, (su san cewa kai bawa ne, Ibn Abbas yace ba'alinsu sun yi shakka mutuwarsa aka fito ttiusu dashi donsu gan shi, har yanzu gangar jikinsa na nan a gidan kayan mu-tanen dana Misra ana zuwa ganinsa) haƙiƙa yawaici daga mutane marabkana ne ga buran ayoyinmu.

93. Haƙiƙa mun saukar da Bani -Isra'ila masaukin gaskiya da karama (shine Sham da Masar[1], mun azurta musu daga dadada, basu sassaba ba (wato ba' alinsu ya bada gaskiya, ba' alinsu yaki bada gaskiya,) saida ilimi yazo musu, haƙiƙa Ubangijinka yana hukunci tsakaninsu da gaskiya a bisa abinda suka kasance suna sassaɓawa a a cikinsa (na daga sha' anin addini, ya tserar da muminai ya azabtar da kafirai).

(GASKIYAR ALKUR' ANI)

94. Idan ka kasance a cikin kokwanto (ya Annabi Muhammadu Sallallahu alaika wasallama) da abinda muka saukar izuwa ga-reka (na daga ƙissoshi ga ƙaddarawa,) to, tambayi waɗanda suke ƙarantawar Attaura na daga gabanka, (sa baka labari da gaskiyarsa, Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama yace "Ni bana kokwanto, bazan tambaya ba") Haƙiƙa gaskiya tazo maka daga Ubangijinka, to, kadaka zamanto daga masu kokwanto (a cikinsa).

95. Kadaka kasance daga waɗanda suka ƙaryatada ayoyin Allah, bare ka zamo daga cikin taɓaɓɓu.

96. Haƙiƙa waɗannan da kalmar Ubangiji ta tabbata a kansu da azaba, bazasu bada gaskiya ba.

97. Koda kowace aya tazo musu, sai sun ga azaba mai raɗaɗi, sannan kuma imani bazai amfane su ba.

1). Masar: An karkata izuwa cewa masar ya Mulka.

فَلَوْلَا كَانَتْ قَرْيَةٌ ءَامَنَتْ فَنَفَعَهَآ إِيمَٰنُهَآ إِلَّا قَوْمَ يُونُسَ لَمَّا
ءَامَنُواْ كَشَفْنَا عَنْهُمْ عَذَابَ ٱلْخِزْيِ فِي ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا وَمَتَّعْنَٰهُمْ
إِلَىٰ حِينٍ ﴿98﴾ وَلَوْ شَآءَ رَبُّكَ لَءَامَنَ مَن فِي ٱلْأَرْضِ كُلُّهُمْ جَمِيعًا
أَفَأَنتَ تُكْرِهُ ٱلنَّاسَ حَتَّىٰ يَكُونُواْ مُؤْمِنِينَ ﴿99﴾ وَمَا كَانَ لِنَفْسٍ
أَن تُؤْمِنَ إِلَّا بِإِذْنِ ٱللَّهِ وَيَجْعَلُ ٱلرِّجْسَ عَلَى ٱلَّذِينَ
لَا يَعْقِلُونَ ﴿100﴾ قُلِ ٱنظُرُواْ مَاذَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ
وَمَا تُغْنِي ٱلْأٓيَٰتُ وَٱلنُّذُرُ عَن قَوْمٍ لَّا يُؤْمِنُونَ ﴿101﴾
فَهَلْ يَنتَظِرُونَ إِلَّا مِثْلَ أَيَّامِ ٱلَّذِينَ خَلَوْاْ مِن قَبْلِهِمْ
قُلْ فَٱنتَظِرُوٓاْ إِنِّي مَعَكُم مِّنَ ٱلْمُنتَظِرِينَ ﴿102﴾ ثُمَّ نُنَجِّي رُسُلَنَا
وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كَذَٰلِكَ حَقًّا عَلَيْنَا نُنجِ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿103﴾
ثمن * قُلْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِن كُنتُمْ فِي شَكٍّ مِّن دِينِي فَلَآ أَعْبُدُ ٱلَّذِينَ
تَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلَٰكِنْ أَعْبُدُ ٱللَّهَ ٱلَّذِي يَتَوَفَّىٰكُمْ
وَأُمِرْتُ أَنْ أَكُونَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿104﴾ وَأَنْ أَقِمْ وَجْهَكَ لِلدِّينِ
حَنِيفًا وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿105﴾ وَلَا تَدْعُ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَنفَعُكَ
وَلَا يَضُرُّكَ فَإِن فَعَلْتَ فَإِنَّكَ إِذًا مِّنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿106﴾

(IMANI BAYA AMFANI YAYIN AZABA

98. Donme alƙarya (wato mutanen alƙarya) basu bada gaskiyaba gaban saukar azaba imaninsu ya amfane su? Sai dai mutanen Annabi Yunusa yayin da suka bada gaskiya yayin ganin azaba basuyi jinkiri har ya sauka ba, mun yaye azabar kunyata ga buransu a cikin rayuwar duniya, mun jiyar dasu daɗi izuwa ƙarewar ajalinsu.
99. Da Ubangijinka yaga dama, da dukkan wanda yake cikin ƙasa saiya bada gaskiya baƙiɗaya. to, shin kaine zaka tilashi mutane da abinda Allah bai nufa ba garesu, har su zamo mumi-nai?(A'a!!).
100. Bazai yiwu watakaita bada gaskiyaba saida izinin Allah, yasanya azaba a kan waɗanda basa hankaltar ayoyin Allah.

(UMARNI DA NAZARI DON SANIN ALLAH DA GARGADI DA ALBISHIR DA KWADAITARWA KAN ILIMI)

101. Cene, "Kuyi duba meye abinda yake cikin sammai da ƙassai (na daga ayoyi masu shiryarwa bisa kaɗaitakar Allah,) ayoyi da manzanni baza suyi amfani ba ga mutanen da basu bada gaskiya da Allah ba. (Domin gargaɗi mumini kaɗai yake amfana)".
102. Masu ƙaryata ka basa sauraron komai illa irin kwanukan waɗanda suka wuce gabansu, (na daga al' umma,) cene, "Ku saurari wannan, ni ina cikin masu sauraro tareda ku.
103. Sannan mu tserar da manzanninmu da waɗanda suka bada gaskiya daga azaba, kamar irin wancananka tserarwa ne, Lalle a kanmu muke tserar da muminai, (Annabi da Sahabbansa, Alaihimassalam).

(KIRA IZUWA MUSULUNCI)

104. Yaku waɗannan mutane in kun kasance cikin shakku daga addinina, to, ni bazan bautawa waɗanda kuke bautawa ba, ba Allah ba, (sune gumaka,) sai dai ni ina bautawa Allah ne wanda yake karɓar rayukanku, an umarce ni in kasance daga muminai.
105. (Ance da ni) "Ka tsayar da fuskata ga addini totar, kadaka kasance daga mushirikai.
106. Kadaka bautawa ba Allah ba abinda bazai amfane ka ba (in baka bauta masua) bazai cuce ka ba (in baka bauta masa ba,) to, in ka aikata wancananka, (takadiran) to, haƙiƙa kai yayin nan kana cikin azzalumai.

وَإِن يَمْسَسْكَ اللَّهُ بِضُرٍّ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥٓ إِلَّا هُوَ ۖ وَإِن يُرِدْكَ بِخَيْرٍ
فَلَا رَآدَّ لِفَضْلِهِۦ ۚ يُصِيبُ بِهِۦ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ ۚ وَهُوَ الْغَفُورُ الرَّحِيمُ ﴿107﴾
قُلْ يَٰٓأَيُّهَا النَّاسُ قَدْ جَآءَكُمُ الْحَقُّ مِن رَّبِّكُمْ ۖ فَمَنِ اهْتَدَىٰ
فَإِنَّمَا يَهْتَدِى لِنَفْسِهِۦ ۖ وَمَن ضَلَّ فَإِنَّمَا يَضِلُّ عَلَيْهَا ۖ وَمَآ أَنَا۠ عَلَيْكُم بِوَكِيلٍ ﴿108﴾
وَاتَّبِعْ مَا يُوحَىٰٓ إِلَيْكَ وَاصْبِرْ حَتَّىٰ يَحْكُمَ اللَّهُ ۚ وَهُوَ خَيْرُ الْحَٰكِمِينَ ﴿109﴾

سُورَةُ هُودٍ مَكِّيَّةٌ 11
وَهِيَ مِائَةٌ وَثَلَاثٌ وَعِشْرُونَ ءَايَةً 122

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

الٓر ۚ كِتَٰبٌ أُحْكِمَتْ ءَايَٰتُهُۥ ثُمَّ فُصِّلَتْ مِن لَّدُنْ حَكِيمٍ خَبِيرٍ ﴿1﴾
أَلَّا تَعْبُدُوٓا۟ إِلَّا اللَّهَ ۚ إِنَّنِى لَكُم مِّنْهُ نَذِيرٌ وَبَشِيرٌ ﴿2﴾ وَأَنِ اسْتَغْفِرُوا۟
رَبَّكُمْ ثُمَّ تُوبُوٓا۟ إِلَيْهِ يُمَتِّعْكُم مَّتَٰعًا حَسَنًا إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى
وَيُؤْتِ كُلَّ ذِى فَضْلٍ فَضْلَهُۥ ۖ وَإِن تَوَلَّوْا۟ فَإِنِّىٓ أَخَافُ عَلَيْكُمْ عَذَابَ يَوْمٍ
كَبِيرٍ ﴿3﴾ إِلَى اللَّهِ مَرْجِعُكُمْ ۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿4﴾
أَلَآ إِنَّهُمْ يَثْنُونَ صُدُورَهُمْ لِيَسْتَخْفُوا۟ مِنْهُ ۚ أَلَا حِينَ يَسْتَغْشُونَ
ثِيَابَهُمْ يَعْلَمُ مَا يُسِرُّونَ وَمَا يُعْلِنُونَ ۚ إِنَّهُۥ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ الصُّدُورِ ﴿5﴾

107. Idan Ubangiji ya same ka da cuta (kamar talauci da rashin Lafiya,) ba mai yaye make sai Allah, in ya nufe ka da alheri, ba mai ije falalarsa, gaburanka yana samun wanda yaga dama da alherinsa, shine mai gafara mai jinƙai.

(TACACCEN ABINDA YA WUCE)

108. Cene, "Yaku mutane, haƙiƙa gaskiya tazo muku daga Ubangijinku, wanda ya shiriya, ya shiriya ne don kansa (don sa-kamakon shiriyar nan nasa ne,) wanda ya ɓata, to, haƙiƙa ya ɓata ne ga kansa kawai, domm masifar ɓatan nan tana kansa,) ni ban kasance wakili a kanku ba (bare in tilashe ku a kan shiriya).

109. Bi abinda ake aikowa izuwa gareka, ka daure a bisa kira zuwa Allah da cutarsu har Allah yayi hukunci cikinsu da abinda yaga dama, shine mafi mahukunta iya hukunci, (yako daure din har Allah yayi hukunci a kan mushirikai da kisa, Ahlul -Kitabi kuma da jiziya).

Suratu Hudu Alaihissalam

A Makka Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Dari Da Ashirin Da Daya (121) Ina farawa dasuna Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabaɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe

(WANNAN SURA TA ƘUNSHI BARAZANA DA BAN KASHI DA RIKON FṢAURI GA ALAMOMIN MASU TAURIN KAI WAƊANDA SUKA WUCE)
(ASALAI NA ADDININ MTISULUNCI MAGAMA)

1.A.L.R, Allah ne masani da abinda yake nufi da wannan kalma, wannan littafi ne da aka inganta ayoyinsa, (da,tsari mai ban mana ki, da ma'anoni masu ƙayatarwa,) sannan aka rabe (hukunce - hukuncentada kissoshinta, da gargaɗe-gargaɗenta filla - filla,) daga gurin Ubangiji; gwani mai cikakken sani.

2. Shine kadaku ,bautawa kowa sai Allah, haƙiƙa ni mai gargaɗi ne garekuda azaba (in kun kafirce ga Allah,) mai albishir ne da sakamako (in kun bada gaskiya).

3. Kuma ku nemi gafarar Ubangijinku (daga shirka da sabo,) sannan ku koma izuwa gareshi (da da'a,) yaji daku ,daɗi a duniya, jiyarwa daɗi kyakkyawa, (da daɗin rayuwa dayalwar arziki,) izuwa ajali abin ambato, (wato mutuwa,) zaiyi baiwa a dukkan mai falala a cikin aiki a Lahira sakamakon falalarsa, idan kun bujire, to, haƙiƙa ni mai jin tsoron rana maigirma ne a gareku, (ranar alƙiyama).

4. Izuwa Allah ne makomarku, shi mai iko ne bisa komai.

(WANI ABU DAGA AYYUKAN KAFIRAI KO MUMINAI MASU -LA' AKARI DA DUBAN ALLAH WATO MASU MURAKABA)

5. To, jama' a haƙiƙa su suna karkatar da ƙirazansu saboda su ɓuya daga Allah, to, jama'a yayin dasuke rufa tufafinsu, Allah yasan abinda suke ɓoyewa da bayyanawa, haƙiƙa Ubangiji masanine da haluluwan ƙirazan bayi.

حزب

۞ وَمَا مِن دَآبَّةٍ فِي الْأَرْضِ إِلَّا عَلَى اللَّهِ رِزْقُهَا وَيَعْلَمُ مُسْتَقَرَّهَا
وَمُسْتَوْدَعَهَا كُلٌّ فِي كِتَابٍ مُّبِينٍ ۝6 وَهُوَ الَّذِي خَلَقَ
السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضَ فِي سِتَّةِ أَيَّامٍ وَكَانَ عَرْشُهُ عَلَى الْمَاءِ
لِيَبْلُوَكُمْ أَيُّكُمْ أَحْسَنُ عَمَلًا وَلَئِن قُلْتَ إِنَّكُم مَّبْعُوثُونَ
مِنْ بَعْدِ الْمَوْتِ لَيَقُولَنَّ الَّذِينَ كَفَرُوا إِنْ هَٰذَا إِلَّا سِحْرٌ
مُّبِينٌ ۝7 وَلَئِنْ أَخَّرْنَا عَنْهُمُ الْعَذَابَ إِلَىٰ أُمَّةٍ مَّعْدُودَةٍ
لَّيَقُولُنَّ مَا يَحْبِسُهُ أَلَا يَوْمَ يَأْتِيهِمْ لَيْسَ مَصْرُوفًا عَنْهُمْ
وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُوا بِهِ يَسْتَهْزِءُونَ ۝8 وَلَئِنْ أَذَقْنَا
الْإِنسَانَ مِنَّا رَحْمَةً ثُمَّ نَزَعْنَاهَا مِنْهُ إِنَّهُ لَيَئُوسٌ كَفُورٌ ۝9
وَلَئِنْ أَذَقْنَاهُ نَعْمَاءَ بَعْدَ ضَرَّاءَ مَسَّتْهُ لَيَقُولَنَّ
ذَهَبَ السَّيِّئَاتُ عَنِّي إِنَّهُ لَفَرِحٌ فَخُورٌ ۝10 إِلَّا الَّذِينَ صَبَرُوا
وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ أُولَٰئِكَ لَهُم مَّغْفِرَةٌ وَأَجْرٌ كَبِيرٌ ۝11
فَلَعَلَّكَ تَارِكٌ بَعْضَ مَا يُوحَىٰ إِلَيْكَ وَضَائِقٌ بِهِ صَدْرُكَ
أَن يَقُولُوا لَوْلَا أُنزِلَ عَلَيْهِ كَنزٌ أَوْ جَاءَ مَعَهُ مَلَكٌ
إِنَّمَا أَنتَ نَذِيرٌ وَاللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ وَكِيلٌ ۝12

(WANI ABU DAGA MABAYYANAR ILIMIN ALLAH DA IKONSA)

6. Babu daga wata mai motsi a cikin ƙasa face arzikinta na kan Ubangiji, ya Lamunce mata dashi don falalarsa, yasan mazaunin ta a duniya da tsatso, yasan gurin ajiye ta bayan ta mutu ko cikin mahaifa, kowane daga abinda aka ambatan nan yana cikin Littafi, wato Lauhul - Mahafuzu.
7. Shine wanda ya halicci sammai da ƙassai a cikin kwanaki shida, da ma can Al'arshinsa gaban halittarsu yana kan ruwa, shine kuma wato ruwan yana kan iska, ya halicce su domin ya jarrabe ku, wannenankune mafi kyakkyawan aiki, wanda yafi bi ga Allah, kuma yaga wanne ne yafi taƙadaranci, Wallahi idan kace dasu, Ya Muhammadu Sallallahu alaika wasallama, haƙiƙa ku ababen tashine bayan mutuwa, Wallahi waɗanda suka kafirta zasu ce; wannan Alƙur'ani mai firici da tashin Alƙiyama bai kasance ba sai tsafi mafi bayyana.

(DABI' O' IN MUTUM DA GYARAN DA ADDINI YAYI MATA)

8. Wallahi idan mun jinkirtada azaba ga buransu izuwa Lokatai ababen kirgawa, Wallahi saisu ce (don izgili kawai,) "Mai ya hana shi sauka", (sai Ubangiji yace;) "To, jama'a ranar dazaizo musu ba abin ijewa ne ba ga buransu, kuma abinda suka kasance suna izgili dashi (na azaba) zai sauka a kansu.
9. Wallahi idan mun ɗanɗanawa mutum rahama daga garemu (wadatada Lafiya,) sannan muka kau da ita daga gareshi, haƙiƙa shi Lalle mai ɗebe hasune daga rahamar Allah, mai yawan butulci ne.
10. Wallahi idan mun ɗanɗana masa daɗi bayan tsananin (talauci da wahala,) Wallahi zaice "Musibu sun tafi ga barina", (bazai saurari gushewarta ko godewarta ba,) haƙiƙa shi mai yawan farin ciki ne, (farin cikin ƙasaita,) mai yawan fariya ne (a kan mutane da abinda aka bashi).
11. Sai waɗanda suka daure a kan wahala sukayi aiki nagari a cikin jin daɗi, waɗannan gafara ta tabbata garesu, da Lada mai girma.

(RARRASHIN ANNABI ALAIHISSALATU WASSA LAMU DA BUWAYA DA ALƘUR' ANI)

12. To, wata ƙila kai! (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama,) mai barin ba'alin abinda aka aiko izuwa gareka ne, (bazaka isar musu dashi ba don wulaƙantarwarsu dashi, kuma ƙirjinka zai kuntata dashi, (da karatunsa a garesu,) donsu ce "Me ya sa ba a saukar da taska a gareshi ba, ko Mala' ika yazo tare dashi (yagasgata shi tamfar yadda muka nema?)" To, kai dai mai gargaɗi ne kawai, ba wani abu a kanka illa ida aike, (ba zuwa da abinda suka shato maka ba,) Allah wakili ne bisa komai (zaiyi musu sakamako ne).

ثمن

أَمْ يَقُولُونَ افْتَرَاهُ قُلْ فَأْتُوا بِعَشْرِ سُوَرٍ مِّثْلِهِ مُفْتَرَيَاتٍ
وَادْعُوا مَنِ اسْتَطَعْتُم مِّن دُونِ اللَّهِ إِن كُنتُمْ صَادِقِينَ ﴿13﴾
فَإِلَّمْ يَسْتَجِيبُوا لَكُمْ فَاعْلَمُوا أَنَّمَا أُنزِلَ بِعِلْمِ اللَّهِ وَأَن لَّا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ
فَهَلْ أَنتُم مُّسْلِمُونَ ﴿14﴾ * مَن كَانَ يُرِيدُ الْحَيَاةَ الدُّنْيَا وَزِينَتَهَا
نُوَفِّ إِلَيْهِمْ أَعْمَالَهُمْ فِيهَا وَهُمْ فِيهَا لَا يُبْخَسُونَ ﴿15﴾ أُولَٰئِكَ الَّذِينَ
لَيْسَ لَهُمْ فِي الْآخِرَةِ إِلَّا النَّارُ وَحَبِطَ مَا صَنَعُوا فِيهَا وَبَاطِلٌ
مَّا كَانُوا يَعْمَلُونَ ﴿16﴾ أَفَمَن كَانَ عَلَىٰ بَيِّنَةٍ مِّن رَّبِّهِ وَيَتْلُوهُ
شَاهِدٌ مِّنْهُ وَمِن قَبْلِهِ كِتَابُ مُوسَىٰ إِمَامًا وَرَحْمَةً
أُولَٰئِكَ يُؤْمِنُونَ بِهِ وَمَن يَكْفُرْ بِهِ مِنَ الْأَحْزَابِ فَالنَّارُ مَوْعِدُهُ
فَلَا تَكُ فِي مِرْيَةٍ مِّنْهُ إِنَّهُ الْحَقُّ مِن رَّبِّكَ وَلَٰكِنَّ
أَكْثَرَ النَّاسِ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿17﴾ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ افْتَرَىٰ
عَلَى اللَّهِ كَذِبًا أُولَٰئِكَ يُعْرَضُونَ عَلَىٰ رَبِّهِمْ وَيَقُولُ الْأَشْهَادُ
هَٰؤُلَاءِ الَّذِينَ كَذَبُوا عَلَىٰ رَبِّهِمْ أَلَا لَعْنَةُ اللَّهِ
عَلَى الظَّالِمِينَ ﴿18﴾ الَّذِينَ يَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ اللَّهِ
وَيَبْغُونَهَا عِوَجًا وَهُم بِالْآخِرَةِ هُمْ كَافِرُونَ ﴿19﴾

13. Haba! Yanzu sa dinga cewa "Ya ƙirƙiri Alƙur'ani, "Cene; "To, kuzo dasurori guda goma irinsa (a cikin fasaha, da gwaninta,) ababen ƙirƙirar, (sabodaku ,Larabawa ne fasihai kamata, saiya buwaye su da waɗannan ayoyi sannan ya neme su dasu zo dasura guda, ya buwaye su da ita,) ku kirawo wanda kuka sami iko ba Allah ba (a kan wannan taimako,) in kun kasance masu gaskiya (a kan cewa ƙirƙira tasa yayi).

14. idan basu amsa muku ba (su waɗannan da kuka kira su saboda taimakon nan,) to, ku mushirikai, an saukar dashine da sanin Allah kawai, (ba ƙirƙirarsa akayi ba,) kuma haƙiƙa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, to, shin, ku ba kwa Musulunta ba ne, (bayan wannan hujja mai yanke hanzari, wato ku Musulunta).

(BARAZANA A KAN WANDA A FIFITA DUNIYA A KAN LAHIRA)

15. Wanda yake nufin rayuwar duniya da kawace - kawacenta zamu cika musu sakamakon aikace - aikacensu, (sadaka, sadar da zumunta,) a cikin duniya, mu yalwata musu arziki, su a cikin duniya baza a tauye musu komai ba.

16. Waɗancananka sune waɗanda basu da komai a Lahira sai wuta, abinda suka aikata shi a cikinta ya watse, (ya zama kurar taga, baza a basu sakamako a kai ba,) abinda suke aikatawa ya kasance banza.

(MASU BADA GASKIYA MASU IMANI DA ALLAH WATO MASU FIFITA LAHIRA A KAN DUNIYA)

17. Yanzu, to, wanda ya kasance a kan bayani daga Ubangijinsa, (shine Annabi Sallallahu alaihi wasallama da muminai wato a kan hujjar alƙur'ani,) kuma mai shaidawa a gareshi, yana bin sa daga Allah, (shine Mala' ika Jibrilu Alaihissalam,) gaban alƙƙur' ani kuma Littafin Annabi Musa (Alaihissalam) shima shaidawa ne a gareshi, halin ka-sancewarsa liman da rahama, zai zama kamar wanda ba haka ba? A'a!) Waɗancananka (waɗanda suka kasance a kan hujja daga Ubangijinsu,) sune suke bada gaskiya da alƙur' ani. Aljanna ta tabbata a garesu, wanda ya kafirce dashi daga ƙungiyoyin kafirai, to, wuTacc alƙawarinsa, kadaka kasance cikin kokwanto daga alƙur'ani, haƙiƙa shi gaskiya ne daga Ubangijinka, amma yawaicin mutane basu bada gaskiyaba [1]

(KAFIRAI DA AYYUKANSU DA SAKAMAKONSU HAKANA MUMINAI)

18. Babu mafi zalunci daga wanda ya ƙirƙiri ƙarya bisa Ubangiji (da dangana shariki ko da a gareshi,) waɗancananka ana bujirar dasu a bisa Ubangijinsu ranar Alƙiyama a cikin jimlar talikai, shaidu zasu shaida, (wato Mala' iku, zasu shaida ga manzanni da iyarwa, ga kafirai kuma da ƙaryatawa, su ce); "Waɗannan sune waɗanda sukayi ƙarya bisa Ubangijinsu, to, jama' a Allah ya tsinewa mushirikai (Amin).

(MASU AMBATON HANYAR ALLAH DA RAJA' IYA SUKE YABON TAKADDUMIN ASARI WATO CI GABAN ZAMANI)

19. Waɗanda suke datsewa ga buran addinin Musulunci, suke neman hanyar addinin Musulunci a karkace, (wato suke kwatanta tada cewa raja'iyace, kuma suke yabon ci gaban zamani a maimakon hanyar Allah) su a Lahira sune kafirai.

1) Kafirai wun fi Musulmi yawa aduniya tun daga daharZuwayanzy.

أُو۟لَٰٓئِكَ لَمْ يَكُونُوا۟ مُعْجِزِينَ فِى ٱلْأَرْضِ وَمَا كَانَ لَهُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ
مِنْ أَوْلِيَآءَ يُضَٰعَفُ لَهُمُ ٱلْعَذَابُ مَا كَانُوا۟ يَسْتَطِيعُونَ
ٱلسَّمْعَ وَمَا كَانُوا۟ يُبْصِرُونَ ﴿20﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓا۟
أَنفُسَهُمْ وَضَلَّ عَنْهُم مَّا كَانُوا۟ يَفْتَرُونَ ﴿21﴾ لَا جَرَمَ
أَنَّهُمْ فِى ٱلْءَاخِرَةِ هُمُ ٱلْأَخْسَرُونَ ﴿22﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟
وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَأَخْبَتُوٓا۟ إِلَىٰ رَبِّهِمْ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَنَّةِ هُمْ فِيهَا
خَٰلِدُونَ ﴿23﴾ ۞ مَثَلُ ٱلْفَرِيقَيْنِ كَٱلْأَعْمَىٰ وَٱلْأَصَمِّ وَٱلْبَصِيرِ وَٱلسَّمِيعِ ربع
هَلْ يَسْتَوِيَانِ مَثَلًا أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ﴿24﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا نُوحًا
إِلَىٰ قَوْمِهِۦٓ إِنِّى لَكُمْ نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿25﴾ أَن لَّا تَعْبُدُوٓا۟ إِلَّا ٱللَّهَ
إِنِّىٓ أَخَافُ عَلَيْكُمْ عَذَابَ يَوْمٍ أَلِيمٍ ﴿26﴾ فَقَالَ ٱلْمَلَأُ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ مِن قَوْمِهِۦ مَا نَرَىٰكَ إِلَّا بَشَرًا مِّثْلَنَا وَمَا نَرَىٰكَ ٱتَّبَعَكَ
إِلَّا ٱلَّذِينَ هُمْ أَرَاذِلُنَا بَادِىَ ٱلرَّأْىِ وَمَا نَرَىٰ لَكُمْ عَلَيْنَا
مِن فَضْلٍۭ بَلْ نَظُنُّكُمْ كَٰذِبِينَ ﴿27﴾ قَالَ يَٰقَوْمِ أَرَءَيْتُمْ
إِن كُنتُ عَلَىٰ بَيِّنَةٍ مِّن رَّبِّى وَءَاتَىٰنِى رَحْمَةً مِّنْ عِندِهِۦ
فَعُمِّيَتْ عَلَيْكُمْ أَنُلْزِمُكُمُوهَا وَأَنتُمْ لَهَا كَٰرِهُونَ ﴿28﴾

20. Wađancananka basu kasance masu tserewa Allah ba a cikin ƙasa, basu da wađansu masu hana musu azabar Allah, ba Allah ba, za a ninninka musu azaba, saboda (sun ɓatar da waninsu bayan batansu,) basu kasance masu samun damar jin gaskiya ba, basu kasance masu ganin gaskiyaba (saboda faifayewar kin su gareta).
21. Wađancananka sune wađanda suka taɓar da kawukansu saboda komawarsu izuwa wuta abar dauwamarwo a garesu, abinda suke ƙirƙira ga Allah (na da'awar sharika) ya bace musu.
22. Ba shakka, haƙiƙa a Lahira sune taɓaɓɓu.
23. Haƙiƙa wađannan da suka bada gaskiya sukayi ayyuka nagargaru, suka tattara tarkacensu izuwa Allah. (wato wađanda ake ce dasu "yan raja' iyya a yanzu, wađanda basu ci gaba ba,) wađancananka sune "yan aljanna, (Allah ka sanya mu cikinsu,) su masu dauwama ne a cikinta.
24. Suffar jama' ar nan guda biyu (kafirai da muminai, to, shi kafiri) kamar makaho da kurma yake, (shi mumini kamar mai ji da gani yake,) Shin sayi daidai a misali? (A' a!) To, donme ba kwa wa' azantuwa.

(ƘISSAR ANNABI NUHU ALAIHISSALAM WACCE TA KUNSHINEMAN GAFARAR UBANGIJI DA TUBA GARESHI SUNE SABABIN SAMUN RUWAN SAMA DA KARFIN DAULA DA SAMUN DUKIYA DA'YA'YA)

25. Haƙiƙa mun aiko Annabi Nuhu (Alaihissalam) izuwa mutanensa, yace (dasu) "Ni mai gargadi ne mabayyanin gargađi a gareku.
26. "Cene kadaku ,bautawa kowa sai Allah, ni ina jin tsoron azabar rana mai rađađi a gareku, (in kun bautawa waninsa)".
27. Sai manyan mutane wađanda suka kafirta daga mutanensa Sukace, "Ba maganinka face mutumne irinmu, Barna ganin wanda yabika face wađanda suke sune wulakantattunmu, marasa zurfin tunani (masaƙa da dukawa,) Bama ganin kuna da wani fifiko a kanmu, Kai! mu muna zaton ku maƙaryata ne (a cikin da' awar jakadanci)".
28. Yace, "Yaku mutanena, ku bani Labari in na kasance bisa bayani daga Ubangijina, ya bani Annabci daga gareshi, ta makanta a gareku, (ita rahamar Annabcin nan,) Shin, ma tilasa muku yarda da ita, alhali ku kuna masu Ki a gareta? (A'a!).

وَيَٰقَوْمِ لَآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ مَالًا اِنْ أَجْرِيَ إِلَّا عَلَى اَ۬للَّهِ وَمَآ أَنَا۠
بِطَارِدِ اِ۬لذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّهُم مُّلَٰقُواْ رَبِّهِمْ وَلَٰكِنِّيَ أَرَيٰكُمْ قَوْمًا
تَجْهَلُونَ ﴿29﴾ وَيَٰقَوْمِ مَنْ يَّنصُرُنِے مِنَ اَ۬للَّهِ إِن طَرَدتُّهُمْ أَفَلَا
تَذَّكَّرُونَ ﴿30﴾ وَلَآ أَقُولُ لَكُمْ عِندِے خَزَآئِنُ اُ۬للَّهِ وَلَآ أَعْلَمُ
اُ۬لْغَيْبَ وَلَآ أَقُولُ إِنِّے مَلَكٌ وَلَآ أَقُولُ لِلذِينَ تَزْدَرِے
أَعْيُنُكُمْ لَنْ يُّوتِيَهُمُ اُ۬للَّهُ خَيْرًا اَ۬للَّهُ أَعْلَمُ بِمَا فِے أَنفُسِهِمْ
إِنِّيَ إِذًا لَّمِنَ اَ۬لظَّٰلِمِينَ ﴿31﴾ ۞ قَالُواْ يَٰنُوحُ قَدْ جَٰدَلْتَنَا فَأَكْثَرْتَ ثمن
جِدَالَنَا فَأْتِنَا بِمَا تَعِدُنَا إِن كُنتَ مِنَ اَ۬لصَّٰدِقِينَ ﴿32﴾
قَالَ إِنَّمَا يَاتِيكُم بِهِ اِ۬للَّهُ إِن شَآءَ وَمَا أَنتُم بِمُعْجِزِينَ ﴿33﴾
وَلَا يَنفَعُكُمْ نُصْحِيَ إِنْ أَرَدتُّ أَنْ أَنصَحَ لَكُمُ إِن كَانَ اَ۬للَّهُ يُرِيدُ
أَنْ يُّغْوِيَكُمْ هُوَ رَبُّكُمْ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿34﴾ أَمْ يَقُولُونَ
اَ۪فْتَرَيٰهُ قُلِ اِنِ اِ۪فْتَرَيْتُهُ فَعَلَيَّ إِجْرَامِے وَأَنَا بَرِےٓءٌ مِّمَّا تُجْرِمُونَ ﴿35﴾
وَأُوحِيَ إِلَيٰ نُوحٍ أَنَّهُ لَن يُّومِنَ مِن قَوْمِكَ إِلَّا مَن قَدْ ءَامَنَ
فَلَا تَبْتَئِسْ بِمَا كَانُواْ يَفْعَلُونَ ﴿36﴾ وَاصْنَعِ اِ۬لْفُلْكَ بِأَعْيُنِنَا
وَوَحْيِنَا وَلَا تُخَٰطِبْنِے فِے اِ۬لذِينَ ظَلَمُوٓاْ إِنَّهُم مُّغْرَقُونَ ﴿37﴾

29. "Yaku mutanena, bana tambayarku Lada bisa ida aike, ni Ladana bai kasance ba sai bisa Ubangiji, ni ba mai kore muminai ne ba, ni ba mai kore wađanda suka bada gaskiya ne ba, (tamfar da kuka umarce ni,) haƙiƙa su, zasu gamu. da Ubangijinsune yayi musu sakamako, yayi sakayya a kansu ga wanda yakore su, sai dai ni, ina ganin ku kuri jahilci ƙarshen al' amarinku.

30. "Yaku mutanena, waye zai ije min azabar Allah in na kore su, Shin, to, ba kwa wa' azantu ba? (Wato ku wa' azantu).

31. "Ni bana ce daku ,taskokin Allah suna gareni, bana cewa na san gaibu, bana cewa ni Mala'ika ne, ni mutumne kamar ku, bana eewa da wađanda idanuwanku ta raina su Allah bai basu alheri ba, Allah ne masani da abinda yake cikin zuka-tansu, haƙiƙa ni, yayin nan in na fađi wannan, Lalle ina daga azzalumai".

(TSANANTAR HALI HAR SUKA NEMI GAGGAUTA AZABA)

32. Sukace "Ya Nuhu kayi jayayya da mu ka yawaita mana jayayya, to, kazo mana da abinda kake mana ban tsoro dashi (na azaba,) in ka kasance daga masu gaskiya".

33. Sai yace, "Allah ne zaizo muku dashi in yaga dama bani ba, ku bazaku tserewa Allah ba.

34. "Nasiha ta bata amfaninku, in na nufi in yi muku nasiha, in ALLah yayi nufin ɓatar da ku, shine Ubangijinku, izuwa gareshi ake komawa da ku".

35. Sai Ubangiji yace, "Haba! donme suke cewa ƙirƙirar Alƙur'ani ma' aiki yayi?" Cene. "In na ƙirƙire shi, to, zunubina yana kaina, ni makubuci ne daga abinda kuke aikatawa (na Laifi)".

(DEBE HASON ANNABI NUHU ALAIHISSALAM DAGA SHIRIYARSU DA SAS SAKAWARSA JIRGI)

36. An aiko izuwa Annabi Nuhu (Alaihissalam) cewa ba mai kuma bada gaskiya daga mutanenka sai wanda ya bada gaskiya, kada kayi baƙin ciki da abinda suka kasance suna aikatawa (na shirka, sai yayi musu mummunar addu'a da fađinsa Ubangiji kadaka bar wani ganzaro a bayan ƙasa, sai Allah ya amsa masa rokonsa).

37. Ubangiji yace (dashi) "Sas saƙa jirgi a maganarmu da kiwonmu, da umarninmu, kada kayi min magana a cikin wađanda sukayi kafirci (da barin halakar dasu,) haƙiƙa su ababen halakarwa ne".

وَيَصْنَعُ اُ۬لْفُلْكَ وَكُلَّمَا مَرَّ عَلَيْهِ مَلَأٌ مِّن قَوْمِهِۦ سَخِرُواْ مِنْهُ
قَالَ إِن تَسْخَرُواْ مِنَّا فَإِنَّا نَسْخَرُ مِنكُمْ كَمَا تَسْخَرُونَ ﴿38﴾
فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ مَن يَأْتِيهِ عَذَابٌ يُخْزِيهِ وَيَحِلُّ عَلَيْهِ عَذَابٌ
مُّقِيمٌ ﴿39﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَ أَمْرُنَا وَفَارَ اَ۬لتَّنُّورُ قُلْنَا اَ۪حْمِلْ فِيهَا
مِن كُلٍّ زَوْجَيْنِ اِ۪ثْنَيْنِ وَأَهْلَكَ إِلَّا مَن سَبَقَ عَلَيْهِ اِ۬لْقَوْلُ
وَمَنْ ءَامَنَ وَمَآ ءَامَنَ مَعَهُۥٓ إِلَّا قَلِيلٌ ﴿40﴾ * وَقَالَ اَ۪رْكَبُواْ فِيهَا
بِسْمِ اِ۬للَّهِ مُجْر۪ىٰهَا وَمُرْسَىٰهَآ إِنَّ رَبِّے لَغَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿41﴾
وَهْيَ تَجْرِے بِهِمْ فِے مَوْجٍ كَالْجِبَالِ وَنَادَىٰ نُوحٌ اِ۪بْنَهُۥ وَكَانَ
فِے مَعْزِلٍ يَٰبُنَيِّ اِ۪رْكَب مَّعَنَا وَلَا تَكُن مَّعَ اَ۬لْكٰفِرِينَ ﴿42﴾
قَالَ سَـَٔاوِے إِلَىٰ جَبَلٍ يَعْصِمُنِے مِنَ اَ۬لْمَآءِ قَالَ لَا عَاصِمَ اَ۬لْيَوْمَ مِنْ
أَمْرِ اِ۬للَّهِ إِلَّا مَن رَّحِمَ وَحَالَ بَيْنَهُمَا اَ۬لْمَوْجُ فَكَانَ مِنَ
اَ۬لْمُغْرَقِينَ ﴿43﴾ وَقِيلَ يَٰٓأَرْضُ اُ۪بْلَعِے مَآءَكِ وَيَٰسَمَآءُ أَقْلِعِے
وَغِيضَ اَ۬لْمَآءُ وَقُضِيَ اَ۬لْأَمْرُ وَاسْتَوَتْ عَلَى اَ۬لْجُودِيِّ وَقِيلَ بُعْداً
لِّلْقَوْمِ اِ۬لظَّٰلِمِينَ ﴿44﴾ وَنَادَىٰ نُوحٌ رَّبَّهُۥ فَقَالَ رَبِّ إِنَّ اَ۪بْنِے مِنْ
أَهْلِے وَإِنَّ وَعْدَكَ اَ۬لْحَقُّ وَأَنتَ أَحْكَمُ اُ۬لْحَٰكِمِينَ ﴿45﴾

ربع

38. Kuma yana Sassaƙa jirgi koyaushe manyan mutanensa suka wuce a gareshi sai suyi izgili dashi, yace, "In kun yi mana izgili , to, haƙiƙa munai muku izgili n nan mu ma, tamfar yadda kuke mana, (idan mun tsira kun nutse).
39. Da sannu zaku san wanda azabaza tazo masa da zata kunyatar dashi, azaba madauwamiya ta sauka a gareshi.
40. To, har Lokacin da al' amarin yazo (da halakar dasu,) tanderun [1] mai gurasa ya ɓarko da ruwa (wannan kuwa alama ne ga Annabi Nuhu Alaihissalam) sai muka ce, "Sanya a cikinta daga dukkan nau'i bi - biyu (namiji da mace, Ance sai Allah ya tara masa namun jeje da tsuntsaye da waninsu, saiya haɗu yana jefa hannayensa biyu a kowane nau' i, saita dama ta faɗa kan namiji, ta hagu ta faɗa kan tam-ata, saiya ajiye su a cikin jirgin) da iyalinka (matarka da "ya"yanka,) sai wanda magana (ta halakarwa) ta rigaya a gareshi.(sune matarsa da ɗansa Kan'ana, banda Samu, Hamu dayafisu, saiya ɗauke su da matayensu uku) da kuma wanda ya bada gaskiya, ba wanda ya bada gaskiya tare dashi sai. kaɗan, (Ance dukkan wanda yake cikin jirgin mutum tamanin ne, arba'in maza, arba" in mata).

41. Annabi Nuhu (Alaihissalam) yace, Ku hau cikinta, kuna masu cewa Bissimillahi maj'raha wamarsaha (kuma Ance zamanin duk da yake so ta motsa sai yace Bissimillahi maj'raha wamarsaha idan kuma yana so ta tsaya saiya faɗi hakan) [2] haƙiƙa Ubangijina Lalle mai gafara ne mai jinƙai (da bai halakar da mu ba). (IYAKAR MUTANEN DA KUMA CETON ANNABI NUHU ALAIHISSALAM GA DANSA)

42. Ita tana gudana dasu a cikin kunfa manya manya kamar duwarwatsu, Annabi Nuhu (Alaihissalam) ya kira ɗansa Kan'an tun jirgi bai motsa ba, ya kasance nesa daga jirgin, yace "Ya kai ɗan nan nawa abin tausayi, hawo tareda mu, kadaka kasance tareda kafirai.
43. Yace da sannu zan tattam izuwa dutse dazai kare ni daga ruwa, Annabi (Nuhu Alaihissalam) yace, ba mai kiyayewa yau daga azabar Allah, sai wanda Allah yajiƙansa, Ubangiji yace, kumfa saita shiga tsakaninsu, ya zama daga cikin ababan nutsarwa.
44. Aka ce, "Yake ƙasa haɗiye ruwanki, (wanda ya Barko daga gareki, to, saita shanye shiya zama shinc a cikin ƙasa ban da wanda ya sakko daga sama, to, shi kuwa ya zama ƙoguna da ƙoramu,) yace, sama kame ga buran ruwa." (saita ƙafe,) aka tauye ruwa aka hukunta al' amari (na halakar mutanen Annabi Nuhu,) ita wannan jirgi ta daidaitu a kan dutsen Judiy (dutse ne a kusa da Mausil' [3], Ance a cikin Hadisi, mutanen farko na wannan al'umma sun risketa [4], kuma da suKafita daga cikin jirgin sun gina wata alƙarya da suka ambace tada madinati samanina, iTace wadda a yanzu ake cewa da ita Babila. akace "Halaka ta tabbata ga mutane kafirai".
45. Annabi Nuhu (Alaihissalam) ya roƙi Ubangijinsa yace, "Ubangiji! Haƙiƙa dana (Kan' anu) yana daga cikin ahalina, ka kumayi alƙawari da tsiransu, haƙiƙa kuma alƙawarinka gaskiya ne, (ba sabawa cikinsa,) alhali kaine mafi iya mahukunta iya hukunci da adalci".

1) A masallacin kufa akwai guri da ake ce masa (mafaratannuri), ance shine wanda Allah yake nufi anan, Allah ne masani. Ni ina ganinsa (wato sarkin yakın shehu Usmanu dan fedio. Shei'kh Muhammadu Nasiru Kabara) lokacin da duk naziyar ci masallacin. 2) Anan ne sayyadina Abdulkadir Jilani yake cewa Bismillahi daga masanin Allah Kamar (Kun) ne daga Allah, - Sanajiy - 3) Wannan dutse ayau yana Icasar Istambul, bakin iyakarsu da kasar Iraq daga kudu kusa da mausil dm. - Sanajiy -) 4) Na Sami labari cewa masu Iktishafi na wannan lokacinma sunhau kan wannan duise sun sa'mi karai rayin ita tuwansa wallahu a'alamu. - Sanajiy -

قَالَ يَٰنُوحُ إِنَّهُۥ لَيْسَ مِنْ أَهْلِكَ إِنَّهُۥ عَمَلٌ غَيْرُ صَٰلِحٍ فَلَا تَسْـَٔلْنِ
مَا لَيْسَ لَكَ بِهِۦ عِلْمٌ إِنِّىٓ أَعِظُكَ أَن تَكُونَ مِنَ ٱلْجَٰهِلِينَ ﴿46﴾
قَالَ رَبِّ إِنِّىٓ أَعُوذُ بِكَ أَنْ أَسْـَٔلَكَ مَا لَيْسَ لِى بِهِۦ عِلْمٌ
وَإِلَّا تَغْفِرْ لِى وَتَرْحَمْنِىٓ أَكُن مِّنَ ٱلْخَٰسِرِينَ ﴿47﴾ قِيلَ يَٰنُوحُ
ٱهْبِطْ بِسَلَٰمٍ مِّنَّا وَبَرَكَٰتٍ عَلَيْكَ وَعَلَىٰٓ أُمَمٍ مِّمَّن مَّعَكَ
وَأُمَمٌ سَنُمَتِّعُهُمْ ثُمَّ يَمَسُّهُم مِّنَّا عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿48﴾ تِلْكَ مِنْ أَنۢبَآءِ
ٱلْغَيْبِ نُوحِيهَآ إِلَيْكَ مَا كُنتَ تَعْلَمُهَآ أَنتَ وَلَا قَوْمُكَ مِن قَبْلِ هَٰذَا
فَٱصْبِرْ إِنَّ ٱلْعَٰقِبَةَ لِلْمُتَّقِينَ ﴿49﴾ ۞ وَإِلَىٰ عَادٍ أَخَاهُمْ هُودًا ثمن
قَالَ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥٓ إِنْ أَنتُمْ
إِلَّا مُفْتَرُونَ ﴿50﴾ يَٰقَوْمِ لَآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ أَجْرًا إِنْ أَجْرِىَ
إِلَّا عَلَى ٱلَّذِى فَطَرَنِىٓ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿51﴾ وَيَٰقَوْمِ ٱسْتَغْفِرُوا۟
رَبَّكُمْ ثُمَّ تُوبُوٓا۟ إِلَيْهِ يُرْسِلِ ٱلسَّمَآءَ عَلَيْكُم مِّدْرَارًا
وَيَزِدْكُمْ قُوَّةً إِلَىٰ قُوَّتِكُمْ وَلَا تَتَوَلَّوْا۟ مُجْرِمِينَ ﴿52﴾
قَالُوا۟ يَٰهُودُ مَا جِئْتَنَا بِبَيِّنَةٍ وَمَا نَحْنُ بِتَارِكِىٓ
ءَالِهَتِنَا عَن قَوْلِكَ وَمَا نَحْنُ لَكَ بِمُؤْمِنِينَ ﴿53﴾

46. Ubangiji yace "Ya Nuhu! Shi baya daga cikin ahalinka, haƙiƙa shi roƙonka gareni da tserar dashi aiki ne ba kyakkyawa ba, saboda shi kafiri ne, kafiri kuma bazai tsira ba a yau, kadaka roƙe ni abinda baka da sani dashi (na tserar da danka,) haƙiƙa ni inayi maka gargaɗi kadaka zama daga cikin marasa sani (da roƙonka abinda baka sani ba)".

47. Annabi Nuhu (Alaihissalam) yace, Ubangiji! Ina neman tsaruwa dakai daga in roƙe ka daga abinda bani sani dashi, in baka gafarce ni ka jiƙaina bana kasance daga taɓaɓɓu".

(ƘARSHEN ƘISSAR DA ABIN) A TAYI NUNI IZUWA GARESHI)

48. Akace "Ya Nuhu! sauka daga wannan jirgi tareda gaisuwa daga garemu da kuma albarkatai a gareka da kuma al 'umma dake taredakai (a cikin jirgi, wato sune na daga "ya"yansu da zuriyarsu, sune muminai, (1) waɗansu al' ummai daga zuriyyar waɗanda suke taredakai kafirai zamu ji dasu daɗi a duniya, sannan azaba mai raɗaɗi ta shafe su a Lahira".

49. Wancananka yana daga Labarin gaibu, muke aiko shi izuwa gareka (Ya Annabi Muhammadu Sallallahu alaika wasallama,) baka kasance ka santa bakai ko mutanenka gaban wannan alƙur'ani, to, daure (a bisa isar da aike, da cutar mutanenka gareka tamfar yadda Annabi Nuhu yadaure,) haƙiƙa kyakkyawan ƙarshe ya tabbata ga masu tsoron Allah.

(ƘISSAR ANNABI HUDU ALAIHISSALAM WACCE TA KUNSHI SHU'UMIN TAURIN AI GA ALLAH DA MANZANNIN SA, ALLAH KIYASHE MU)

50. Mun aiko Annabi Hudu (Alaihissalam) izuwa Adu (dan uwansu na ƙabila,) yace, "Yaku mutanena ku bautawa Allah, bakuda wani abin bautawa ba Allah ba, ku baku kasance ba a cikin bautar gumaka face maƙaryata.

51. "Yaku mutanena, bana tambayarku Lada (bisa ida aike,) Ladana bai kasance ba illa bisa wanda ya halicce ni, yanzu ba kwayi hankali ba?

52. "Yaku mutanena ku nemi gafarar Ubangijinku daga dukkan zunubi (daya wuce,) ku tuba izuwa gareshi (da curuwa da kudurin aniyar rashin komawa,) ya sako ruwa a gareku, (da can ko an hana su ruwan,) mai yawan kwarara a gareku, ya ƙara muku ƙarfi a kan ƙarfinku, (dukiya da "ya"ya,) kadaku ,bada baYakuna masu Laifi".

53. Sukace, "Ya Hudu! bakazo mana da wani dalili a bisa maganarka ba, mu bazamubar iyayen gijinmu don maganarka ba, mu bazamu bada gaskiya don kai ba!

(1) Wannan kirari da Allah yayi ga waɗanda suke .cikin jirgi musamman "ya"ya yen Annabi Nuhu guda Uku, ya hana ace Annabi Nuhu ya la'anci dayansu, bayan kirarin da Allah yayi masu gabadaya, saboda haka hadisin da aka samu na cevva Annabi Nuhu ya la'anci dansa Hamu bai sami tushe a alƙur'ani ba, wato wannan Hadisaida makamantansu na masu t'ifita launine akan launi ballantana in an dubi aya mai cewa : (Inna akra makum indallahi atkakum.) wato mafi girman ku wurin Ubangiji shine wanda yafi ku Tsoran sa. - Sanajiy -

إِن نَّقُولُ إِلَّا ٱعْتَرَىٰكَ بَعْضُ ءَالِهَتِنَا بِسُوٓءٍ قَالَ إِنِّىٓ أُشْهِدُ
ٱللَّهَ وَٱشْهَدُوٓا۟ أَنِّى بَرِىٓءٌ مِّمَّا تُشْرِكُونَ مِن دُونِهِۦ
فَكِيدُونِى جَمِيعًا ثُمَّ لَا تُنظِرُونِ ﴿54﴾ إِنِّى تَوَكَّلْتُ عَلَى ٱللَّهِ
رَبِّى وَرَبِّكُم مَّا مِن دَآبَّةٍ إِلَّا هُوَ ءَاخِذٌۢ بِنَاصِيَتِهَآ إِنَّ رَبِّى
عَلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿55﴾ فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَقَدْ أَبْلَغْتُكُم مَّآ أُرْسِلْتُ بِهِۦٓ إِلَيْكُمْ
وَيَسْتَخْلِفُ رَبِّى قَوْمًا غَيْرَكُمْ وَلَا تَضُرُّونَهُۥ شَيْـًٔا إِنَّ رَبِّى عَلَىٰ
كُلِّ شَىْءٍ حَفِيظٌ ﴿56﴾ وَلَمَّا جَآءَ أَمْرُنَا نَجَّيْنَا هُودًا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مَعَهُۥ
بِرَحْمَةٍ مِّنَّا وَنَجَّيْنَٰهُم مِّنْ عَذَابٍ غَلِيظٍ ﴿57﴾ وَتِلْكَ عَادٌ جَحَدُوا۟
بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمْ وَعَصَوْا۟ رُسُلَهُۥ وَٱتَّبَعُوٓا۟ أَمْرَ كُلِّ جَبَّارٍ عَنِيدٍ ﴿58﴾
وَأُتْبِعُوا۟ فِى هَٰذِهِ ٱلدُّنْيَا لَعْنَةً وَيَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ أَلَآ إِنَّ عَادًا كَفَرُوا۟ رَبَّهُمْ
أَلَا بُعْدًا لِّعَادٍ قَوْمِ هُودٍ ﴿59﴾ وَإِلَىٰ ثَمُودَ أَخَاهُمْ صَٰلِحًا قَالَ يَٰقَوْمِ
ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥ هُوَ أَنشَأَكُم مِّنَ ٱلْأَرْضِ وَٱسْتَعْمَرَكُمْ
فِيهَا فَٱسْتَغْفِرُوهُ ثُمَّ تُوبُوٓا۟ إِلَيْهِ إِنَّ رَبِّى قَرِيبٌ مُّجِيبٌ ﴿60﴾
۞ قَالُوا۟ يَٰصَٰلِحُ قَدْ كُنتَ فِينَا مَرْجُوًّا قَبْلَ هَٰذَآ أَتَنْهَىٰنَآ أَن نَّعْبُدَ
مَا يَعْبُدُ ءَابَآؤُنَا وَإِنَّنَا لَفِى شَكٍّ مِّمَّا تَدْعُونَآ إِلَيْهِ مُرِيبٍ ﴿61﴾

ربع

54. Mu bamu cewa komai acikin sha'anin ka sai ɗai ba' alin iyayen gijinmune ya shafe daka mummuna, (ya ɓata hankalinka saboda zagin da kake musu,)" yace, "Ni ina shaidarwa Allah, ku shaida haƙiƙa ni makuɓuci ne daga abinda kuke tara Allah dashi (a cikin bauta ba Allah ba,) to, kuyi dabara a cikin halakar dani bakiɗayanku, (kuda gumakanku,) sannan kada kuyi mini sauraro.

55. "Haƙiƙa ni, na dogara bisa Allah Ubangijina, Ubangijinku, babu daga wata mai motsi a bayan ƙasa face Ubangiji ne mariƙi ga makawarkwaɗarta, ai mana llaki ne gareta, ba amfani ba cuta saida izininsa, haƙiƙa Ubangijina yana kan tafarki madaidaici, totar kan gaskiya da adalci.

56. "To, in kun bada baya, haƙiƙa na iyar muku abinda aka aiko ni dashi zuwa gareku, Ubangijina zai kawo waɗansu mutanen baku ba, baza kn cuce shi komai ba. Haƙiƙa Ubangijina mai kiwo ne bisa komai".

57. Yayin da azabarmu tazo sai muka tserar da Annabi Hudu (Alaihissalam) da waɗanda suka bada gaskiya tare dashi, da rahama daga garemu, muka tserar dasu daga azaba mai kauri.

58. Wancananka Adu ne, sun yi musun ayoyin Ubangijinsu, sun sabi manzonninsa, sun bi umarnin dukkan jabberi mai taurin kai.

59. An biyar musu da tsinewa a cikin wannan duniya, ranar Lahira kuma za a biyar musu da tsinewa (bisa talikai,) to, jama' a, haƙiƙa Adu sun kafirce wa Ubangijinsu, to, jama' a, nisa daga rahamar Allah ya tabbata ga Adawa mutanen Annabi Hudu. (Allah ya kiyashemu Amin).

(ƘISSAR ANNABI SALIHU ALAIHIS-SALAM TAREDA SHU'UMIN TAU-RIN KAU GA ALLAH DA MANZAN NIN SA WANDA WANNAN ƘISSA DA IRINTA - IRINTA SUKA ƘUNSA)

60. Mun aiko Annabi Salihu (Alaihissalam) izuwa Samudawa (ɗan uwansu na ƙabilarsu.) yace, "Yaku mutanena! Ku kaɗaita Allah, bakuda wani Ubangiji bashi ba, shine ya fari halittarku daga ƙasa, (ta wajen halittar ubanku Annabi Adamu Alaihissalam daga gareta [1] yasanya ku masu rayatada zama a cikinta, ku nemi gafararsa (daga dukkan zunubai, sannan ku tuba izuwa gareshi (da curuwa da ɗaure azama a kan baza a koma ba,) haƙiƙa Ubangijina makusanci ne (da halittada saninsa) mai amsawa wanda ya roƙe shine.

61. Sukace, "Ya Salihu (Alaihissalam,) haƙiƙa ka kasance a cikinmu abin ƙaunar ka zama shugaba gaban wannan abu ɗa ya faru daga gareka, yanzu ka dinga hana mu mu bautawa abinda iyayenmu suke bautawa (na gumaka,) haƙiƙa mu muna cikin kokwanto a bisa abinda kake kiranmu izuwa gareshi na tauhidi mai afkurwa cikin shakka".

1) Anan Allah ya ƙaryata"yan tunanin ƙarya masu cewa mutum ya faru ne daga biri da saunan irin haukansu - Sanajiy

قَالَ يَٰقَوْمِ أَرَآيْتُمُۥٓ إِن كُنتُ عَلَىٰ بَيِّنَةٍ مِّن رَّبِّيَ وَءَاتَىٰنِي مِنْهُ رَحْمَةً
فَمَنْ يَنصُرُنِي مِنَ اللَّهِ إِنْ عَصَيْتُهُۥ فَمَا تَزِيدُونَنِي غَيْرَ تَخْسِيرٍ ﴿62﴾
وَيَٰقَوْمِ هَٰذِهِۦ نَاقَةُ اللَّهِ لَكُمُۥٓ ءَايَةً فَذَرُوهَا تَأْكُلْ فِي أَرْضِ اللَّهِ
وَلَا تَمَسُّوهَا بِسُوٓءٍ فَيَأْخُذَكُمْ عَذَابٌ قَرِيبٌ ﴿63﴾ فَعَقَرُوهَا
فَقَالَ تَمَتَّعُواْ فِي دَارِكُمْ ثَلَٰثَةَ أَيَّامٍ ذَٰلِكَ وَعْدٌ غَيْرُ مَكْذُوبٍ ﴿64﴾
فَلَمَّا جَآءَ أَمْرُنَا نَجَّيْنَا صَٰلِحًا وَالَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ بِرَحْمَةٍ مِّنَّا
وَمِنْ خِزْيِ يَوْمَئِذٍ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ الْقَوِيُّ الْعَزِيزُ ﴿65﴾
وَأَخَذَ الَّذِينَ ظَلَمُواْ الصَّيْحَةُ فَأَصْبَحُواْ فِي دِيَٰرِهِمْ
جَٰثِمِينَ ﴿66﴾ كَأَن لَّمْ يَغْنَوْاْ فِيهَآ أَلَآ إِنَّ ثَمُودَاْ كَفَرُواْ رَبَّهُمُۥٓ
أَلَا بُعْدًا لِّثَمُودَ ﴿67﴾ وَلَقَدْ جَآءَتْ رُسُلُنَا إِبْرَٰهِيمَ بِالْبُشْرَىٰ
قَالُواْ سَلَٰمًا قَالَ سَلَٰمٌ فَمَا لَبِثَ أَن جَآءَ بِعِجْلٍ حَنِيذٍ ﴿68﴾
فَلَمَّا رَءَآ أَيْدِيَهُمْ لَا تَصِلُ إِلَيْهِ نَكِرَهُمْ وَأَوْجَسَ
مِنْهُمْ خِيفَةً قَالُواْ لَا تَخَفْ إِنَّآ أُرْسِلْنَآ إِلَىٰ قَوْمِ
لُوطٍ ﴿69﴾ وَامْرَأَتُهُۥ قَآئِمَةٌ فَضَحِكَتْ فَبَشَّرْنَٰهَا
بِإِسْحَٰقَ وَمِن وَرَآءِ إِسْحَٰقَ يَعْقُوبَ ﴿70﴾

62. Yace, Yaku mutanena! Ku bani Labari in na kasance a kan bayani daga Ubangijina, ya bani rahama (Annabci) daga gareshi, waye mai hana min azabar Allah in na saɓe shi, baku ƙara mini komai saitaɓewa.

63. "Yaku mutanena! Wannan taguwar Allah ce a gareku halin kasancewarta tana aya, ku barta tayi kiwo a cikin ƙasar Allah, kadaku ,shafe tada mugu, (sarewa) sai azaba makusanciya ta same ku.

64. To, sai suka soketa (wato ƙudaru yasoketada umarninsu,) sai Annabi Salihu (Alaihissalam) yace, kuji daɗi a gidanku kwana uku, (sannan ku halaka,) wancananku alƙawari ne ba ƙarya cikinsa.

65. Yayin da umarninmu yazo (da halakar dasu,) sai muka tserar da Annabi Salihu (Alaihissalam) tareda waɗanda suka bada gaskiya tare dashi (su dubu huɗu) da rahama daga garemu, muka tserar dasu daga kunyar wannan rana, haƙiƙa Ubangijinka shine ƙaƙƙarfa, mabuwayi.

66. Tsawa ta kama waɗanda suka zalunci kansu suka zama halakakku a cikin gidajensu, suna durƙushe (a kan gwuiwoyinsu matattu).

67. Kamar su basu taɓazama a cikin gidajensu ba, Kai'. haƙiƙa Samudawa sun kafircewa Ubangijinsu, kai! nisa daga rahamar Allah ya tabbata ga Samudawa. (Allah ya kiyashemu, Amin).

(ƘISSAR ANNABI IBRAHIM ALAIHISSALAM DA KUMA GIRMAMA BAƘI)

68. Haƙiƙa manzanninmu sun zowa Annabi Ibrahim (Alaihissalam) da albishir (da Ishaka da yaƙuba bayansa,) Sukace, "Gaisuwa" yace, "Gaisuwa a gareku." bai daɗe ba sai yazoda ɗan maraƙi soyayye.

69. Yayin da yaga hannuwansu basa saduwa izuwa gareshi, saiya mushesu ya ɗarsa tsoro daga garesu a cikin zuciyarsa, (suka fahinci haka,) Sukace, "Kada kaji tsoro, mu an aiko mune izuwa mutanen Annabi Luɗu (Alaihissalam) ne don mu halakar dasu".

70. Matarsa (Saratu tana tsaye tanayi musu hidima,) to, saitayi dariya (don farinciki da halakarsu,) sai mukayi mata albishir da Ishaƙa, bayan Ishaƙa kuma Yakuba. (An haifi Ishaƙa bayan bushara da shekara ɗaya, Isma' ila ya girme shi da shekara goma sha huɗu).

ثمن

قَالَتْ يَٰوَيْلَتَيٰٓ ءَآلِدُ وَأَنَا عَجُوزٞ وَهَٰذَا بَعْلِي شَيْخًاۖ
إِنَّ هَٰذَا لَشَيْءٌ عَجِيبٞۖ ﴿71﴾ قَالُوٓاْ أَتَعْجَبِينَ مِنْ أَمْرِ اِ۬للَّهِۖ رَحْمَتُ
اُ۬للَّهِ وَبَرَكَٰتُهُۥ عَلَيْكُمُۥٓ أَهْلَ اَ۬لْبَيْتِۖ إِنَّهُۥ حَمِيدٞ مَّجِيدٞۖ ﴿72﴾
* فَلَمَّا ذَهَبَ عَنْ إِبْرَٰهِيمَ اَ۬لرَّوْعُ وَجَآءَتْهُ اُ۬لْبُشْرَيٰ يُجَٰدِلُنَا فِي قَوْمِ
لُوطٍۖ ﴿73﴾ إِنَّ إِبْرَٰهِيمَ لَحَلِيمٌ أَوَّٰهٞ مُّنِيبٞۖ ﴿74﴾ يَٰٓإِبْرَٰهِيمُ أَعْرِضْ عَنْ هَٰذَآۖ
إِنَّهُۥ قَدْ جَآءَ أَمْرُ رَبِّكَۖ وَإِنَّهُمُۥٓ ءَاتِيهِمْ عَذَابٌ غَيْرُ مَرْدُودٖۖ ﴿75﴾ وَلَمَّا
جَآءَتْ رُسُلُنَا لُوطٗا سِيٓءَ بِهِمْ وَضَاقَ بِهِمْ ذَرْعٗا وَقَالَ هَٰذَا
يَوْمٌ عَصِيبٞۖ ﴿76﴾ وَجَآءَهُۥ قَوْمُهُۥ يُهْرَعُونَ إِلَيْهِ وَمِن قَبْلُ كَانُواْ يَعْمَلُونَ
اَ۬لسَّيِّـَٔاتِۖ قَالَ يَٰقَوْمِ هَٰٓؤُلَآءِ بَنَاتِي هُنَّ أَطْهَرُ لَكُمْۖ فَاتَّقُواْ اُ۬للَّهَ
وَلَا تُخْزُونِ فِي ضَيْفِيٓۖ أَلَيْسَ مِنكُمْ رَجُلٞ رَّشِيدٞۖ ﴿77﴾ قَالُواْ لَقَدْ
عَلِمْتَ مَا لَنَا فِي بَنَاتِكَ مِنْ حَقّٖ وَإِنَّكَ لَتَعْلَمُ مَا نُرِيدُۖ ﴿78﴾
قَالَ لَوْ أَنَّ لِي بِكُمْ قُوَّةً أَوْ ءَاوِيٓ إِلَيٰ رُكْنٖ شَدِيدٖۖ ﴿79﴾
قَالُواْ يَٰلُوطُ إِنَّا رُسُلُ رَبِّكَ لَن يَصِلُوٓاْ إِلَيْكَۖ فَاسْرِ بِأَهْلِكَ
بِقِطْعٖ مِّنَ اَ۬ليْلِ وَلَا يَلْتَفِتْ مِنكُمُۥٓ أَحَدٌ إِلَّا اَ۪مْرَأَتُكَۖ إِنَّهُۥ مُصِيبُهَا
مَآ أَصَابَهُمُۥٓۖ إِنَّ مَوْعِدَهُمُ اُ۬لصُّبْحُۖ أَلَيْسَ اَ۬لصُّبْحُ بِقَرِيبٖۖ ﴿80﴾

71. Tace, "Ya kaicona! Ƙaƙa za tayiwu in haihu ina tsohuwa ('yar shekara ɗari ɗaya - babu,) wannan mijina yana tsoho (ɗan shekara ɗari ko da ashirin,) haƙiƙa wannan abin mana ki ne ƙwarai". Shine asamu ɗa daga tso faf fi guda biyu.

72. Sukace, "Kyayi mana ki daga al'amarin Allah, rahamar Allah da albarkatansa sun tabbata a gareku, Yaku "yan ɗakin Annabi Ibrahim (Alaihissalatu - wassalam,) haƙiƙa Ubangiji shine abin godewa, maigirma".

73. Yayin da tsoro ya kau ga Annabi Ibrahim (Alaihissalamu) albishir (da haihuwa) yazo masa, saiya haɗu yana jayayya da manzanninmu (wannan shine Hausawa suke cewa daɗin goyo shiya kawo zunkudo).

74. Haƙiƙa Annabi Ibrahim (Alai-hissalamu) Lalle) mai yawan nutsuwa ne, mai yawan faɗin Ah![1] mai yawan komawa da al'amari izuwa Allah ne, (Yace dasu kwa halakar da alƙarya da muminai ɗari uku yake ciki, sukace a'a, muminai maitan fa, sukace a'a, arba' in fa, sukace a'a, goma sha huɗu fa, sukace a'a ɗaya fa, sukace a'a, sai yace akwai Annabi Luɗu Alaihissalam a ciki, sukace ai mu mun san ko suwaye a ciki. Yayin daya tsawaita musu sai suka ce):

75. Ya Ibrahim (Alaihissalamu) rabu da wannan jayayya, haƙiƙa wannan laniari, umarnin Ubangijinka ne da halakar dasu yazo, Lalle su waɗannan mutane azaba ba abar juyarwa batazo musu.

76. Yayin da jakadunmu suka zowa Annabi Luɗu (Alaihissalam,) sai yayi baƙin ciki saboda su, ƙirjinsa ya ƙuntata dasu, (saboda kyan fuskarsu a cikin surar baƙi, yaji tsoron mutanensa a garesu,) yace, "Wannan rana ce mai tsanani".

77. Ilai kuwa! sai mutanensa sukazo suna gaggawa izuwa gareshi, tun kafin zuwansu kuma sun ka sance suna aikata miyagun ayyuka, (zowa mazata bayansu) yace, "Yaku mutanena, waɗannan "ya"yana ne mata, su sun fi tsarki gareku ku auresu, ku tsoraci Allah kadaku ,kunyata ni cikin baƙina, shin ba wani mutum shiryayye a cikinku! (dazaiyi umarni da aikin alheri yayi hani ga buran aikin munkari?)".

78. Sukace, "Lalle kasan bamu da wata bukata a cikin "ya" yanka, mata haƙiƙa kai, kasan abinda muke nufi, (na zaikewa maza)".

79. Yace, "Ina ma ina da ƙarfi a tareda ku, ko in tattaro izuwa rukuni mai ƙarfi, (wato dangi da zasu taimake ni, to da nai muku ruƙon tsauri. "Waɗannan baƙin Mala' iku kuwa sun yi Lamfa).

80. Yayin da Mala'iku suka ga wannan, sai Sukace, "Ya Annabi Luɗu,,haƙiƙa mu jakadun Ubangijinka ne! Bazasu iya saduwa izuwa gareka da mu ba, sai ka tafi da iyalinka a yankin dare, kada ɗaya daga cikinku yayi waiwaye, (don kada ya ga gurungunɗimin abindazai sauka a garesu,) sai matarka, (kadata fita tareda ku,) don abindazai same su, zai same ta, (ta fito tayi waiwaye tace, "Wayyo mutanena" sai wani dutse yazo ya rangaɗeta) ya tambayi baƙin ga Lokacin halakar mutanen, sukace Lokacin halakar mutanen, sukace Lokacin Sudai asubahi ne, "yace," "Ina son wanda yafi wannan gaggawa" Sukace,) "Yanzu asuba ba makusanciyaba ce.?

1) Ah! Ah! wato zikirin Amfasu acikin Alƙur'ani Kamar yadda yagabata - Sanajiy -

فَلَمَّا جَآءَ أَمْرُنَا جَعَلْنَا عَٰلِيَهَا سَافِلَهَا وَأَمْطَرْنَا عَلَيْهَا
حِجَارَةً مِّن سِجِّيلٍ مَّنضُودٍ ﴿82﴾ مُّسَوَّمَةً عِندَ رَبِّكَ وَمَا هِيَ
مِنَ الظَّٰلِمِينَ بِبَعِيدٍ ﴿83﴾ ۞ وَإِلَىٰ مَدْيَنَ أَخَاهُمْ شُعَيْبًا قَالَ
يَٰقَوْمِ اعْبُدُوا اللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُ وَلَا تَنقُصُوا
الْمِكْيَالَ وَالْمِيزَانَ إِنِّي أَرَىٰكُم بِخَيْرٍ وَإِنِّي أَخَافُ عَلَيْكُمْ
عَذَابَ يَوْمٍ مُّحِيطٍ ﴿84﴾ وَيَٰقَوْمِ أَوْفُوا الْمِكْيَالَ وَالْمِيزَانَ بِالْقِسْطِ
وَلَا تَبْخَسُوا النَّاسَ أَشْيَآءَهُمْ وَلَا تَعْثَوْا فِي الْأَرْضِ مُفْسِدِينَ ﴿85﴾
بَقِيَّتُ اللَّهِ خَيْرٌ لَّكُمْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿86﴾ وَمَا أَنَا
عَلَيْكُم بِحَفِيظٍ ﴿87﴾ قَالُوا يَٰشُعَيْبُ أَصَلَوَٰتُكَ تَأْمُرُكَ
أَن نَّتْرُكَ مَا يَعْبُدُ ءَابَآؤُنَا أَوْ أَن نَّفْعَلَ فِي أَمْوَٰلِنَا
مَا نَشَٰٓؤُاْ إِنَّكَ لَأَنتَ الْحَلِيمُ الرَّشِيدُ ﴿88﴾ قَالَ يَٰقَوْمِ
أَرَءَيْتُمْ إِن كُنتُ عَلَىٰ بَيِّنَةٍ مِّن رَّبِّي وَرَزَقَنِي
مِنْهُ رِزْقًا حَسَنًا وَمَآ أُرِيدُ أَنْ أُخَالِفَكُمْ إِلَىٰ
مَآ أَنْهَىٰكُمْ عَنْهُ إِنْ أُرِيدُ إِلَّا الْإِصْلَٰحَ مَا اسْتَطَعْتُ
وَمَا تَوْفِيقِيٓ إِلَّا بِاللَّهِ عَلَيْهِ تَوَكَّلْتُ وَإِلَيْهِ أُنِيبُ ﴿89﴾

حزب

81. Yayin da umarninmu yazoda halakar dasu, sai muka sanya samancin alƙaryatunsu ƙasancinta, (shine Mala' ika Jibrilu Alaihissalam ya daga ta izuwa sama ya kifar da ita a juye izuwa ƙasa,) muka saki ruwan duwatsu a ƙansu na ƙonannan yimbu.

82. Mai bi - biya abar alamtawa (dasunan wandaza a jefa da ita,) nan ga Ubangijinka, ita waɗannan garuruwa bata kasance mai nisa bada garin kafi-rai mutanen Makka (1)

(ƘISSAR ANNABI SHA' AIBU ALAIHISSALAMU WACCETA ƘUNSHI HANI DA TAUYE MA' AUNI DA MUDU)

83. Mun aiko Annabi Sha'aibu (Alaihissalam) izuwa Madayana (ɗan uwansa a ƙabila,) yace, "Yaku mutanena ku bautawa Allah, bakuda wani abin bautawa bashi ba, kadaku ,tauye mudu da ma'auni, ni ina ganinkuda alheri, (ni' ima zata wadatar daku ,ga buran tauye mudu,) ni, ina jin tsoron ranar azaba mai kewayewa gareku, (in baku bada gaskiya ba).

84. "Yaku mutanena ku cika mudu da ma'auni da adalci, kadaku ,tauyewa mutane kayansu, kada kuyi ɓarna a bayan kasa. kada kuyi ɓarna

85. "Rara ta Ubangiji (wato arzikinsa mai wanzuwa garekune bayan kun cika mudu da ma'auni) shi yafi amfani gareku daga tauyewa) in kun kasance muminai.

86. "Ni,,ban kasance mai tsaro a gareku ba (in saka mukuda aikinku,) ni mai gargadi ne kawai".

87. Suka faɗa gareshi (don izgili ,) "Ya Sha' aibu, shin sallolinka ne suke umarninka da mubar abinda iyayenmu suke bautawa, (na gumaka,) ko mubar abinda muka gadama a cikin dukiyoyinmu, haƙiƙa kai, kaine mai nutsuwa shiryayye" (Sun faɗi wannan don ba'a).

88. Yace, "Yaku mutanena ku bani Labari in na kasance a kan bayani daga Ubangijina, ya azurta ni arziki kyakkyawa daga gareshi (na halal,) yanzu na cuɗanya shi da haram? shine in tauye ma'auni,) ni bana nufin in saba muku, in je zuwa abinda na hane ku ga buransa, ni, bana nufin komai sai gyara (garekuda adalci,) gwargwadon ikona, gamdakatar dina bai kasance ba saida taimakon Allah, a gareshi na dogara, zuwa gareshi nake komawa.

1) Ubangiji yace, ba mai nisa ce ba ga mutanen Makka, a yanzu kuma ta zama ba mai nisa ce badaga kowa, saboda kowa yake so ya ziyarci waɗannan gurare yana saduwa da ita ba tareda wahala ba cikin "yan sa' o' i, munjajje dai! Allah ya sa izna ta amt'ane mu,. Amin). - Sanajiy -

وَيَٰقَوْمِ لَا يَجْرِمَنَّكُمْ شِقَاقِيَ أَن يُصِيبَكُم مِّثْلُ مَآ أَصَابَ
قَوْمَ نُوحٍ أَوْ قَوْمَ هُودٍ أَوْ قَوْمَ صَٰلِحٍ وَمَا قَوْمُ لُوطٍ
مِّنكُم بِبَعِيدٍ ﴿89﴾ وَاسْتَغْفِرُوا رَبَّكُمْ ثُمَّ تُوبُوا إِلَيْهِ إِنَّ رَبِّي
رَحِيمٌ وَدُودٌ ﴿90﴾ قَالُوا يَٰشُعَيْبُ مَا نَفْقَهُ كَثِيرًا مِّمَّا تَقُولُ
وَإِنَّا لَنَرَىٰكَ فِينَا ضَعِيفًا وَلَوْلَا رَهْطُكَ لَرَجَمْنَٰكَ وَمَا أَنتَ
عَلَيْنَا بِعَزِيزٍ ﴿91﴾ قَالَ يَٰقَوْمِ أَرَهْطِيَ أَعَزُّ عَلَيْكُم مِّنَ اللَّهِ
وَاتَّخَذتُّمُوهُ وَرَآءَكُمْ ظِهْرِيًّا إِنَّ رَبِّي بِمَا تَعْمَلُونَ مُحِيطٌ ﴿92﴾
وَيَٰقَوْمِ اعْمَلُوا عَلَىٰ مَكَانَتِكُمْ إِنِّي عَامِلٌ سَوْفَ تَعْلَمُونَ
مَن يَأْتِيهِ عَذَابٌ يُخْزِيهِ وَمَنْ هُوَ كَٰذِبٌ وَارْتَقِبُوا إِنِّي
مَعَكُمْ رَقِيبٌ ﴿93﴾ * وَلَمَّا جَآءَ أَمْرُنَا نَجَّيْنَا شُعَيْبًا وَالَّذِينَ
ءَامَنُوا مَعَهُ بِرَحْمَةٍ مِّنَّا وَأَخَذَتِ الَّذِينَ ظَلَمُوا الصَّيْحَةُ
فَأَصْبَحُوا فِي دِيَٰرِهِمْ جَٰثِمِينَ ﴿94﴾ كَأَن لَّمْ يَغْنَوْا فِيهَا
أَلَا بُعْدًا لِّمَدْيَنَ كَمَا بَعِدَتْ ثَمُودُ ﴿95﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا
مُوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَا وَسُلْطَٰنٍ مُّبِينٍ ﴿96﴾ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ وَمَلَإِيْهِ
فَاتَّبَعُوا أَمْرَ فِرْعَوْنَ وَمَا أَمْرُ فِرْعَوْنَ بِرَشِيدٍ ﴿97﴾

ثمن

89. "Yaku mutanena, kada saɓa min ya sabauta muku, cewa misalin abinda ya sami mutanen Annabi Nuhu ya same ku, ko mutanen Annabi Hudu ko mutanen Annabi Salihu, mutanen Annabi Luɗu basu kasance manisanta daga gamruwanku ba.

90. ku nemi gafarar ubaginkuda tubadaga dukkan zunubai sannan ku tuba izuwa gareshi, da ciruwa ga buran zunubai da nadama a kan abinda ya wuce da azama a kan rashin komawa. haƙiƙa ubangijina mai jinƙai ne ga muminai mai ƙaunar su ne.

91. Sukace, (don sanarwa da rashin kulawa); "Ya Sha' aibu Barna fahintar yawaici daga abinda kake faɗa, mu muna ganinka rarrauna a cikinmu, ba don danginka bada mun jefe ka, kai baka kasance maigirma a garemu ba".

92. Yace, "Ya mutanena, yanzu jama'aTace tafi girma a gareku daga Allah, ku ka riƙe shi abin jefarwa a bayanku? Haƙiƙa Ubangijina mai kewayewa ne da abinda kuke aikatawa.

93. "Yaku mutanena kuyi aiki bisa halinku, ni mai aiki ne bisa halina, da sannu zaku san wanda azabazata kunyatar-dashi za tazo masa da wanda yake makaryaci, ku saurari ƙarshen Lamarinku, haƙiƙa ni mai sauraro ne taredaku ,.

94. Yayin da umarninmu yazo (da halakar dasu,) sai muka tserar da Annabi Sha' aibu (Alaihissalam) da waɗanda suka bada gaskiya dashi da rahama daga garemu, tsawar (Mala' ika Jibrilu Alaihissalamu) ta kama waɗanda suka cuci kawukansu, sai suka zama halakakku a kan gwuiwoyinsu a cikin gidaddajinsu.

95. Kai kace kamar basu taɓazama a cikinta ba, kai jama' a, nisa daga rahamar Allah ya tabbata ga Madayyanu, tamfar da Samudawa suka nisanta.

(WANI ABU DAGA ƘISSAR ANNABI MUSA ALAIHISSALAM DA FIR' AUN WACCE TA ƘUNSHI JA GORAN - CIN SA IZUWA WUTA.)

96/97. Haƙiƙa mun aiko Annabi Musa (Alaihissalam) izuwa Fir' auna da hujjoji mabayyana ga manyan mutanensa. Al'amarin Fir' auna bashiryayye ne ba.

يَقْدُمُ قَوْمَهُۥ يَوْمَ ٱلْقِيَـٰمَةِ فَأَوْرَدَهُمُ ٱلنَّارَ وَبِئْسَ ٱلْوِرْدُ
ٱلْمَوْرُودُ ﴿98﴾ وَأُتْبِعُوا۟ فِى هَـٰذِهِۦ لَعْنَةً وَيَوْمَ ٱلْقِيَـٰمَةِ بِئْسَ
ٱلرِّفْدُ ٱلْمَرْفُودُ ﴿99﴾ ذَٰلِكَ مِنْ أَنۢبَآءِ ٱلْقُرَىٰ نَقُصُّهُۥ عَلَيْكَ
مِنْهَا قَآئِمٌ وَحَصِيدٌ ﴿100﴾ وَمَا ظَلَمْنَـٰهُمْ وَلَـٰكِن ظَلَمُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ
فَمَآ أَغْنَتْ عَنْهُمْ ءَالِهَتُهُمُ ٱلَّتِى يَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ
مِن شَىْءٍ لَّمَّا جَآءَ أَمْرُ رَبِّكَ وَمَا زَادُوهُمْ غَيْرَ تَتْبِيبٍ ﴿101﴾
وَكَذَٰلِكَ أَخْذُ رَبِّكَ إِذَآ أَخَذَ ٱلْقُرَىٰ وَهِىَ ظَـٰلِمَةٌ
إِنَّ أَخْذَهُۥٓ أَلِيمٌ شَدِيدٌ ﴿102﴾ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَةً لِّمَنْ خَافَ عَذَابَ ٱلْـَٔاخِرَةِ
ذَٰلِكَ يَوْمٌ مَّجْمُوعٌ لَّهُ ٱلنَّاسُ وَذَٰلِكَ يَوْمٌ مَّشْهُودٌ ﴿103﴾ وَمَا نُؤَخِّرُهُۥٓ
إِلَّا لِأَجَلٍ مَّعْدُودٍ ﴿104﴾ * يَوْمَ يَأْتِ لَا تَكَلَّمُ نَفْسٌ إِلَّا بِإِذْنِهِۦ
فَمِنْهُمْ شَقِىٌّ وَسَعِيدٌ ﴿105﴾ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ شَقُوا۟ فَفِى ٱلنَّارِ لَهُمْ فِيهَا
زَفِيرٌ وَشَهِيقٌ ﴿106﴾ خَـٰلِدِينَ فِيهَا مَا دَامَتِ ٱلسَّمَـٰوَٰتُ وَٱلْأَرْضُ
إِلَّا مَا شَآءَ رَبُّكَ إِنَّ رَبَّكَ فَعَّالٌ لِّمَا يُرِيدُ ﴿107﴾
وَأَمَّا ٱلَّذِينَ سُعِدُوا۟ فَفِى ٱلْجَنَّةِ خَـٰلِدِينَ فِيهَا مَا دَامَتِ ٱلسَّمَـٰوَٰتُ
وَٱلْأَرْضُ إِلَّا مَا شَآءَ رَبُّكَ عَطَآءً غَيْرَ مَجْذُوذٍ ﴿108﴾

ربع

98. Zaiyi wa mutanensa jagora ranar Alƙiyama ya shigar dasu wuta, tir! wannan gangara abar gangarawa.
99. An biyar musu da tsinewa a cikin wannan duniya, ranar alƙiyama, tir da wannan taimako abin taimakawa! (taimakon wannan la' ana da akayi daɗi kan ta farko).

(IZNA DA GARGADI DAGA ƘISSOSHI DA AZABAR DUNIYA)

100. Wancananka yana daga labaran alƙaryatu da muke Labarta maka (Ya Annabi Muhammadu Sallallahu alaika wasallama,) akwai daga gareta garin da yake a tsaye, (mutanensa sun halaka, shi yana nan) akwai daga gareta wanda yake a girbe wato ya halaka (mutanen sun halaka, ba wata alama ta su ko tasa kamar hatsin da aka girbe).
101. Bamu zalunce su ba (da halakar dasu bada zunubi ba,) sai dai sun zalunci kansune (dashirka da sabo,) iyayen gijin nan nasu dasuke bautawa basu wadatar musu da komai ba wanin Allah, yayin da al' amarin Ubangijinka yazo (na azaba,) basu kara musu komai bada bautar dasuke musu sai tabarwa.
102. Kamar wancananka damƙa ne, damƙar Ubangijinka, yayin daya damƙi mutanen garuruwa alhali ita tana azzaluma (da zunubai,) ba wani abu daya amfane su daga damkar Allah, haƙiƙa ríkon Ubangiji mai raɗadi ne mai tsananine (Buhari da Muslim sun ruwaito ga Abu Musal -ash' ari, haƙiƙa Ubangiji yana jinkiri ga azzalumi har yayin da in ya rike shi bazai kubce masa ba).

(GARGADI MAGAMI A CIKIN WAƊANNAN ƘISSOSHI)

103. Haƙiƙa a cikin wancananka (na daga waɗannan Labarai) akwai izina ga wanda yake tsoron azabar Lahira, wancananka ranar Lahira, rana ce abar tarawar mutane cikinta, wancananka rana ce abar halarta (ga dukkan talikai, zasu halarce ta).
104. Ba majinkirta ta sai izuwa lok-aci abin kirgawa sananne gun Allah.

(ZURFAFAN HAƘIƘOƘI NA CIKIN ALƘUR' ANI)

105. Ranar da wancananka rana zata zo, ba wani mutumin dazaice ƙala! saida izinin Ubangiji, akwai daga cikinsu tnatsiyaci, akwai daga cikinsu mai arziki, (wato dan wutada dan aljanna).
106. amma matsiyata (a cikin sanin allah,) to, suna cikin wuta, ƙaraji da shassheka ya tabbata garesu a cikinta.
107. madauwama a cikinta, muddin dauwamar sammai da ƙassai a duniya, sai abinda allah ya nufa (na daga kari a kan muddar tasu daga abinda bashi da iyaka, wato madauwama ne a cikinta har abada,) haƙiƙa ubangijinka mai aikatawa ne da abinda yake so.
108. amma waɗanda suka azurta , to, suna cikin aljanna, masu dauwa-ma a cikinta muddar dauwamar sammai da ƙassai, sai abinda Ubangijinka ya nufa (na daga kari,) baiwa ba abar yankewa ba.

فَلَا تَكُ فِي مِرْيَةٍ مِّمَّا يَعْبُدُ هَٰٓؤُلَآءِ مَا يَعْبُدُونَ إِلَّا كَمَا
يَعْبُدُ ءَابَآؤُهُم مِّن قَبْلُ وَإِنَّا لَمُوَفُّوهُمْ نَصِيبَهُمْ غَيْرَ مَنقُوصٍ ﴿109﴾
وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَى ٱلْكِتَٰبَ فَٱخْتُلِفَ فِيهِ وَلَوْلَا كَلِمَةٌ سَبَقَتْ
مِن رَّبِّكَ لَقُضِيَ بَيْنَهُمْ وَإِنَّهُمْ لَفِي شَكٍّ مِّنْهُ
مُرِيبٍ ﴿110﴾ وَإِنَّ كُلًّا لَّمَّا لَيُوَفِّيَنَّهُمْ رَبُّكَ أَعْمَٰلَهُمْ إِنَّهُ بِمَا
يَعْمَلُونَ خَبِيرٌ ﴿111﴾ فَٱسْتَقِمْ كَمَآ أُمِرْتَ وَمَن تَابَ مَعَكَ
وَلَا تَطْغَوْاْ إِنَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿112﴾ وَلَا تَرْكَنُوٓاْ إِلَى ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ
فَتَمَسَّكُمُ ٱلنَّارُ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِنْ أَوْلِيَآءَ
ثُمَّ لَا تُنصَرُونَ ﴿113﴾ وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ طَرَفَيِ ٱلنَّهَارِ وَزُلَفًا مِّنَ ٱلَّيْلِ
إِنَّ ٱلْحَسَنَٰتِ يُذْهِبْنَ ٱلسَّيِّـَٔاتِ ذَٰلِكَ ذِكْرَىٰ
لِلذَّٰكِرِينَ ﴿114﴾ وَٱصْبِرْ فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يُضِيعُ أَجْرَ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿115﴾
فَلَوْلَا كَانَ مِنَ ٱلْقُرُونِ مِن قَبْلِكُمْ أُوْلُواْ بَقِيَّةٍ
يَنْهَوْنَ عَنِ ٱلْفَسَادِ فِي ٱلْأَرْضِ إِلَّا قَلِيلًا مِّمَّنْ أَنجَيْنَا مِنْهُمْ
وَٱتَّبَعَ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مَآ أُتْرِفُواْ فِيهِ وَكَانُواْ مُجْرِمِينَ ﴿116﴾
وَمَا كَانَ رَبُّكَ لِيُهْلِكَ ٱلْقُرَىٰ بِظُلْمٍ وَأَهْلُهَا مُصْلِحُونَ ﴿117﴾

(FIRGITARWA DA TABBATARWA)

109. To, kadaka zama Ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama a cikin kokwanto daga abinda wađannan suke bautawa (na gumaka,) mu zamu yi, musu azabane tamfar da muka azabci wađanda suke gabansu, (wan-nan rarrashine ga manzon Allah sallallahu alaihi wasallama,) basa yin bauta sai kamar yadda iyayensu suke bauta tun gaba, alhali kuwa munyi musu azaba, hakika mu zamu cika musu rabonsu cikakke ba abin tauyewa ba.

110. Hakika mun baiwa annabi Musa (Alaihissalam) Attaura sai aka sassaba a cikinsa (da gasgatawa da karyatawa a cikinsa kamar alkur' ani,) ba don kalma data rigaya daga Ubangijinka (da jinkirin sakamako Izuwa ranar Alkiyama badajinkirin azaba,) da an yi hukunci tsakaninsu (a duniya) a cikin abinda suka sassaba a cikinsa, hakika su suna cikin kokwanto mai afkarwa a cikin tuhuma.

111. Hakika kowanne daga talikai, hakika Ubangiji zai cika musu sakamakonsu, hakika shi Ubangiji mai cikakken sanine da abinda suke aikatawa.

ISTIKAMA A TSORORUWAR DARAJAR TA

112. Tsaya kyam! (a kan aiki da alkur ani da kira izuwa Allah) kamar yadda aka umarce ka, wanda ya bada gaskiya taredakai (shima yayi kyam kamar haka,) kada kuyi shisshigi, Ubangiji masanine da abinda kuke aikatawa.

113. kadaku ,karkata izuwa wađanda sukayi zalunci, (saboda soyayyako almundahana) sai wuta ta kona ku, bakuda wađansu masu tsare ku daga azabar Allah ba Allah ba, sannan baza a hana muku azabar Allah ba.

(TSAIDA SALLOLI BIYAR DA HAKURI)

114. Bada salla cikakkiya gefe biyu narana, (wato asuba, azahar, la'asar,) dayanki na dare, (wato magariba,lisha,) hakika kyawawan ayyuka (kamarsalloli biyar) suna tafi da miyagun,ayyuka, (ta sauka cikin wanda yasunbaci wata mace ba tasa ba, sai manzon Allah ya bashi labarsai yace,to, nine kađai nake da wannan? ko kuwa dukkan al'umma ? sai manzon Allah sallalahu alaihi wasallama yace a'a ga jukkan al'umma tane, Buhari da Muslim sun ruwaito shi) wancananka gargađi ne ga masu wa'azantuwa.

115. Daure bisa cutar mutanenka da aikini bada, da saukar bala'i, hakika Ubangiji baya tozarta ladan masu aiki.

(SABABI MAGAMI A CIKIN HALAKAR DA AL'UMMA WACCE TA GABATA)

116. Yanzu ba a sami ma'abuta hankali da addini daga tsaraiku wađanda suke gabanku suyi hani ga buran barna abayan kasa ba sai kađan daga wađanda muka tserar daga garesu, sun yi hani suka tsira,wađanda sukayi zalunci (da barna da barin hani) sun bi abinda akani'imta su a cikinsa, suka zama mutane ma'abuta laifi..

117. Ubangijinka bai kasance yana halakar da alkarya don zaluntarta daga gareshi da ita alhali mutanenta suna mutanen kirki.

وَلَوْ شَآءَ رَبُّكَ لَجَعَلَ النَّاسَ أُمَّةً وَاحِدَةً وَلَا يَزَالُونَ مُخْتَلِفِينَ
إِلَّا مَن رَّحِمَ رَبُّكَ وَلِذَٰلِكَ خَلَقَهُمْ وَتَمَّتْ كَلِمَةُ رَبِّكَ لَأَمْلَأَنَّ جَهَنَّمَ
مِنَ الْجِنَّةِ وَالنَّاسِ أَجْمَعِينَ ﴿118﴾ * وَكُلًّا نَّقُصُّ عَلَيْكَ مِنْ أَنۢبَآءِ الرُّسُلِ ثمن
مَا نُثَبِّتُ بِهِۦ فُؤَادَكَ وَجَآءَكَ فِي هَٰذِهِ الْحَقُّ وَمَوْعِظَةٌ وَذِكْرَىٰ
لِلْمُؤْمِنِينَ ﴿119﴾ وَقُل لِّلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ اعْمَلُوا عَلَىٰ مَكَانَتِكُمْ إِنَّا عَامِلُونَ ﴿120﴾
وَانتَظِرُوا إِنَّا مُنتَظِرُونَ ﴿121﴾ وَلِلَّهِ غَيْبُ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَإِلَيْهِ
يُرْجَعُ الْأَمْرُ كُلُّهُۥ فَاعْبُدْهُ وَتَوَكَّلْ عَلَيْهِ وَمَا رَبُّكَ بِغَافِلٍ عَمَّا تَعْمَلُونَ ﴿122﴾

12 سُورَةُ يُوسُفَ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ مِائَةٌ وَإِحْدَىٰ عَشْرَةَ ءَايَةً 111

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

الٓر تِلْكَ ءَايَٰتُ الْكِتَٰبِ الْمُبِينِ ﴿1﴾ إِنَّا أَنزَلْنَٰهُ قُرْءَٰنًا عَرَبِيًّا
لَّعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿2﴾ نَحْنُ نَقُصُّ عَلَيْكَ أَحْسَنَ الْقَصَصِ
بِمَا أَوْحَيْنَا إِلَيْكَ هَٰذَا الْقُرْءَانَ وَإِن كُنتَ مِن قَبْلِهِۦ لَمِنَ الْغَٰفِلِينَ ﴿3﴾
إِذْ قَالَ يُوسُفُ لِأَبِيهِ يَٰٓأَبَتِ إِنِّي رَأَيْتُ أَحَدَ عَشَرَ
كَوْكَبًا وَالشَّمْسَ وَالْقَمَرَ رَأَيْتُهُمْ لِي سَٰجِدِينَ ﴿4﴾

118. Da Ubangijinka yaga dama da sai yasanya mutane al'umma ɗaya, (a cikin addini daya,) bazasu gushe ba masu sassabawa a cikin addini sai wanda Ubangijinka yajiƙansa, saboda haka ya halicce su, (ya halicci ma'abuta sabawa don sabawa ma'abuta rahama donrahama,) kalmar Ubangiji ka ta cika,(itace) Lalle zan cika jahannama da mutum da aljan bakiɗaya

(AMFANIN ƘISSOSHI)

119. Muna labartamaka dukkan abinda ake bukata izuwa gareshi na daga labarin manzanni, wato abinda muke tabbatar da zuciyar ka dashi ta nutsu, gaskiya tazo maka(a cikin waɗannan labaru) da gargaɗi da tunatarwa ga muminai.

120. Faɗi ga waɗannan da basa bada gaskiya, kuyi aiki a kan halinku, haƙiƙa mu masu aiki ne (a kan halinmu,firgitarwa ne garesu,) ku saurari ƙarshen al'amarinku, haƙiƙa mu,masu sauraron (wancananka ne)

121. Gaibin sammai da ƙassaina ga Allah,zuwa gareshi ake komo da al'amari dukkansa, (ya azabci wanda ya sabe shi,) saika bautamasa (shi kaɗai,) ka dogara a gareshi,Ubangijinka bai kasance marabkani ba gaburan abinda suke aikatawa.

Suratu Yusufu Alaihissalam

A Makka Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Dari Da Goma Sha Daya (111)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabaɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe.

(wannan sura ta ƙunshi kyan dacewa da munasabada abinda yake gabanta na ƙissoshin Annabawa da fasaha, dayadda ake yin zaren- gwana a babobin balaga da ƙarfafar Manzon Allah sallallahu alaihiwasallama da bashi labarin Annabi Yusufu Alaihissalam,da mana kan duniya da iznace-iznace, da ɗabi'ar dan Adann,kamar son ɗa da hassada tsakanin "yan" uwa,da yaudarar waɗansu,dayadda mutum yake amsawa kiran dabi'a, da nada-ma, da hikimomi, da fadodin sarakuna,da masarautu, da malamai, da haƙuri kan bala'i, da dauriya,da sanin fassarar mafarki, dasauran irinsu cikin mafi kyan tsari, mafi arafinyancinsa, (Subuhanallahi,) Allah da girma yake, alƙur'ani da balaga yake, lalle daga Allah yake.)

(ƘISSAR ANNABI YUSUFU ALAIHISSALAM)

1.A,L.R. (Allah ne masani da wannan kal-ma), waɗancananka waɗannan ayoyin alƙur'anine mai bayyana ƙarya da gaskiya.

2. Haƙiƙa mu, mun saukar dashi kur'ani balarabe, donku al'ummar Annabi kuyi hankali.

(MAFI KYAN LABARTAWA)

3. Mu, muna labarta maka mafi kyan labartawa da aikowarmu wannan Alƙur'ani izuwa gareka, haƙiƙa ka kasance gabansa kana daga mawofuntan tunani.

ANNABI YUSUFU ALAIHISSALAMU A CIKIN FAGEN ƘURUCIYA TAREDA MAHAIFINSA ALHALI YAYI MAFARKI)

4. ka ambata zamanin da Annabi Yusufu yake faɗa ga mahaifinsa,(Alaihimassalam,) "Ya babana! Ni,na ga a mafarkina tauraro goma sha daya da rana da wata, na gansu sunamasu sajada a gareni".

قَالَ يَٰبُنَيَّ لَا تَقۡصُصۡ رُءۡيَاكَ عَلَىٰٓ إِخۡوَتِكَ فَيَكِيدُواْ لَكَ كَيۡدًاۖ
إِنَّ ٱلشَّيۡطَٰنَ لِلۡإِنسَٰنِ عَدُوّٞ مُّبِينٞ 5 وَكَذَٰلِكَ يَجۡتَبِيكَ
رَبُّكَ وَيُعَلِّمُكَ مِن تَأۡوِيلِ ٱلۡأَحَادِيثِ وَيُتِمُّ نِعۡمَتَهُۥ عَلَيۡكَ وَعَلَىٰٓ
ءَالِ يَعۡقُوبَ كَمَآ أَتَمَّهَا عَلَىٰٓ أَبَوَيۡكَ مِن قَبۡلُ إِبۡرَٰهِيمَ وَإِسۡحَٰقَۚ
إِنَّ رَبَّكَ عَلِيمٌ حَكِيمٞ 6 لَّقَدۡ كَانَ فِي يُوسُفَ وَإِخۡوَتِهِۦٓ
ءَايَٰتٞ لِّلسَّآئِلِينَ 7 إِذۡ قَالُواْ لَيُوسُفُ وَأَخُوهُ أَحَبُّ إِلَىٰٓ أَبِينَا مِنَّا
وَنَحۡنُ عُصۡبَةٌ إِنَّ أَبَانَا لَفِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٍ 8 ٱقۡتُلُواْ يُوسُفَ أَوِ ٱطۡرَحُوهُ
أَرۡضٗا يَخۡلُ لَكُمۡ وَجۡهُ أَبِيكُمۡ وَتَكُونُواْ مِنۢ بَعۡدِهِۦ قَوۡمٗا
صَٰلِحِينَ 9 ۞ قَالَ قَآئِلٞ مِّنۡهُمۡ لَا تَقۡتُلُواْ يُوسُفَ وَأَلۡقُوهُ ربع
فِي غَيَٰبَتِ ٱلۡجُبِّ يَلۡتَقِطۡهُ بَعۡضُ ٱلسَّيَّارَةِ إِن كُنتُمۡ فَٰعِلِينَ 10
قَالُواْ يَٰٓأَبَانَا مَا لَكَ لَا تَأۡمَ۫نَّا عَلَىٰ يُوسُفَ وَإِنَّا لَهُۥ
لَنَٰصِحُونَ 11 أَرۡسِلۡهُ مَعَنَا غَدٗا يَرۡتَعۡ وَيَلۡعَبۡ وَإِنَّا لَهُۥ
لَحَٰفِظُونَ 12 قَالَ إِنِّي لَيَحۡزُنُنِيٓ أَن تَذۡهَبُواْ بِهِۦ وَأَخَافُ
أَن يَأۡكُلَهُ ٱلذِّئۡبُ وَأَنتُمۡ عَنۡهُ غَٰفِلُونَ 13 قَالُواْ
لَئِنۡ أَكَلَهُ ٱلذِّئۡبُ وَنَحۡنُ عُصۡبَةٌ إِنَّآ إِذٗا لَّخَٰسِرُونَ 14

5. Yace, "Ya kai ɗan yarona, kadaka labarta mafarkinka ga"yan uwanka sai suyi maka kaidi, kaidi, (suyi dabara a cikin halakar dakai don hassada saboda sun san fassarar mafarkin. sune taurari,mahaifiyarka rana,ni mahaifinka wata,) haƙiƙa shaiɗan magauci ne mabayyanin kiyayyaga mutum.
6. "Hakana, kamar yaddaka gani dinnan hakana Ubangijinka yake zaɓinka, yake sanar dakai daga fassarar mafarki, ya cika ni'ima a gareka (da Annabci) da kuma "ya"yan Annabi Yaƙubu (Alaihissalamu,) tamfar daya cika ta(da Annabci) a bisa ga iyayenka guda biyu tun gaba, Annabi Ibrahim da Annabi Ishaƙu (Alaihimussalamu,) Haƙiƙa Ubangijinka masanine gwani ne).

(YUSUFU ALAIHISSALAMU TAREDA "YAN"UWANSA)

7. Haƙiƙa iznace - iznace ga masu tambayo,ya kasance a cikin labarin AnnabiYusufu (Alaihissalamu) da "yan" uwansa(goma sha ɗaya) ga masu tambayo.
8. Ka ambata zamanin da suka faɗa, (wato ba'alin "yan'uwan ya faɗa ga ba'ali,) Lalle Yusufu da ɗan uwansa (Buniyaminu) su sukafi soyuwa ga ubanmu daga mu,alhali mu, muna jama'a haƙiƙa babanmu yana cikin kuskure mabayyani (dayafifita su a kanmu.)
9. "Ku kashe Yusufu, koku jefa shi rijiyamai nisa, fuskar babanku ta tsarkaka gareku, (yaso ku, ku kadai,) ku zama bayan kashe shi ko jefar dashi mutane ne na kirki, (wato, ku tuba)".
10. Sai wani daga cikinsu ya faɗa (shine Yahuda,) "kadaku ,kashe Yusufu kudai ku jefa shi a cikin zuɗuɗun tsohuwar rijiya,ba'alin matafiyaya tsince shi. in kun kasance masu aikata (abinda kuka nufa na rarrabawa tsakaninsa da ubansa, to, ku isu da wannan)".

("YAN" UWAN ANNABI YUSUFU ALAIHISSALAM SUNA NUFIN ZA SUYI MASA KAIDI KUMA SUYI HANZARI)

11. Sukace, "ya babanmu, meke gareka baka amince mana ba a bisa Annabi Yusufu (Alaihi-ssalam,) haƙiƙa mu masu nasiha ne gareshi, (masu tsayawa da masalahohinsa.)
12. Sake shi tareda mu gobe (izuwa jeji,)mu yi kiwo mu yi wasa, haƙiƙa mu, ,masu kiyayewa ne gareshi}.
13. Yace "Haƙiƙa ni, yana baƙanta minciki ku tafi dashi, (bana son rabo dashi,) ina jin tsoron kura ta cinye shi, alhali ku marabkana ne ga buransa".
14. Sukace, "Wallahi idan kura ta cinye shi,alhali mu muna kungiya, haƙiƙa mutaɓaɓɓu ne" (yayin nan saiya sake shi tare dasu.

فَلَمَّا ذَهَبُواْ بِهِۦ وَأَجْمَعُوٓاْ أَن يَجْعَلُوهُ فِي غَيَٰبَٰتِ ٱلْجُبِّ وَأَوْحَيْنَآ
إِلَيْهِ لَتُنَبِّئَنَّهُم بِأَمْرِهِمْ هَٰذَا وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿15﴾ وَجَآءُوٓ أَبَاهُمْ
عِشَآءً يَبْكُونَ ﴿16﴾ قَالُواْ يَٰٓأَبَانَآ إِنَّا ذَهَبْنَا نَسْتَبِقُ وَتَرَكْنَا
يُوسُفَ عِندَ مَتَٰعِنَا فَأَكَلَهُ ٱلذِّئْبُ وَمَآ أَنتَ بِمُؤْمِنٍ لَّنَا
وَلَوْ كُنَّا صَٰدِقِينَ ﴿17﴾ وَجَآءُو عَلَىٰ قَمِيصِهِۦ بِدَمٍ كَذِبٍ قَالَ بَلْ
سَوَّلَتْ لَكُمْ أَنفُسُكُمْ أَمْرًا فَصَبْرٌ جَمِيلٌ وَٱللَّهُ ٱلْمُسْتَعَانُ عَلَىٰ
مَا تَصِفُونَ ﴿18﴾ وَجَآءَتْ سَيَّارَةٌ فَأَرْسَلُواْ وَارِدَهُمْ فَأَدْلَىٰ دَلْوَهُۥ
قَالَ يَٰبُشْرَىٰ هَٰذَا غُلَٰمٌ وَأَسَرُّوهُ بِضَٰعَةً وَٱللَّهُ عَلِيمٌۢ بِمَا يَعْمَلُونَ ﴿19﴾
وَشَرَوْهُ بِثَمَنٍۭ بَخْسٍ دَرَٰهِمَ مَعْدُودَةٍ وَكَانُواْ فِيهِ
مِنَ ٱلزَّٰهِدِينَ ﴿20﴾ وَقَالَ ٱلَّذِي ٱشْتَرَىٰهُ مِن مِّصْرَ
لِٱمْرَأَتِهِۦٓ أَكْرِمِي مَثْوَىٰهُ عَسَىٰٓ أَن يَنفَعَنَآ
أَوْ نَتَّخِذَهُۥ وَلَدًا وَكَذَٰلِكَ مَكَّنَّا لِيُوسُفَ فِي ٱلْأَرْضِ
وَلِنُعَلِّمَهُۥ مِن تَأْوِيلِ ٱلْأَحَادِيثِ وَٱللَّهُ غَالِبٌ عَلَىٰٓ أَمْرِهِۦ
وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿21﴾ ۞ وَلَمَّا بَلَغَ أَشُدَّهُۥٓ
ءَاتَيْنَٰهُ حُكْمًا وَعِلْمًا وَكَذَٰلِكَ نَجْزِي ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿22﴾

ثمن

15. A yayin da suka tafi dashi, sai suka kulle cewa su jefa shi a cikin zuđuđun kummmar rijiya, (wacce take a Maƙami Annabi Yakuba a farsahi na uku, ana kiran wurin Nabulsa a yau,(to, sai suka saka shi bayan sun tuɓe ri-garsa sun doke shi sun wulaƙanta shi sun nufi kashe shi, suka zura shi, yayin daya sadu izuwa tsakiyar rijiyar saisuka sake shi donya mutu, saiya fađa a cikin ruwa, saiya tattara izuwa watafa, sai suka kira shiya amsa musu yana zaton za sujikansa, suka nufi ragwargwazashi da fa, Yahuza ya hana su.) Muka aiko izuwa gareshi, a cikin kururruma wahayina haƙiƙa (yana dan shekara goma sha ba kwai,) lalle zaka basu labari (bayan yau) da aikinsu wannan, alhali su basu san kaine ba (a halin bada labari!)

16/17. To, Suka zowa basanau lok-acin lisha suna kukan ƙarya Sukace, "Ya babanmu, mu mun tafi muna harbi, mun bar yusufu nan ga tufafinmu sai kura ta cinye shi, kai bazaka gaskatamu ba, ko da mun kasance magasgata.

18. Sukazo a bisa rigarsa dajini na ƙarya,(suka yanka makyarara suka birshine tada jininta, suka mance basu tsaga ba,Annabi Yaƙubu Alaihissalama, yace, yayin dayaganta lafiyayyiya yasan ƙaryarsu,) "ku dai kanku ta ƙawata muku al'amari ne kawai, to, al'amarina haƙuri ne mai kyau, Allah ne abin neman taimako bisa abinda kuke kwatantawa".

19. Matafiya (wato ayari ne na Larabawa) sukazo (daga madayana izuwa Misra, suka sauka kusa da wannan rijiya, a rana ta biyu,)sai suka aiko dan ganganimansu, Maluku dan Zu'urual-Huza'i, saiya jefa gugansa (acikin rijiya, sai Annabi Yusufu Alaihissalamu ya kama igiyar, sai yafito dashi,yayin dayagan shi) sai yace "Ya albishirina, wannan yaro, mai daraja", sai "yan uwansa sukayi sani dashi, sukazo gunsa, suka ɓoye al'amarinsa, suna masu ,sanyashi abin sayarwa, (sukace "Wannan bawanmune daya gudu", shi kuma Annabi Yusufu Alaihissalamu yayi shiru don kar su kashe shi,) Allah masanine da abinda suke aikatawa.

20. Suka sayi Annabi Yusufu daga "yan'uwansa da tamani wulakantacce, dirhamomi ababan ƙirgawa, (ashirin ko ashirin da biyu,) sun kasance suna masu kyama a cikinsa.

21. (Sai matafiyan nan sukazo dashi Misra, sai wanda ya saye shiya sayar dashi da dinare ashirin da takalmi biyu da tufa biyu,) wanda ya saye shi daga Misra (shine ƙdifiru Ma'ajin Misra, ya saye shi don mata tasa Zaliha,) yace "girmama mazauninsa nan gareki ko ya amfane mu, ko mu riƙe shi da." Tamfar da muka tserar dashi daga kisa da jefawa a rijiya muka hore masa zuciyar Ma'ajin Misra, ƙidifiru, hakana muka bunƙasar dashi Annabi Yusufu (Alaihissalam a kasar Misra,) kuma don mu sanar dashi daga fassarar mafarkai, Allah mai rinjaye ne a kan lamarinsa, (ba abinda yake gajiyar dashi,) sai dai yawaicin mutane basu san haka ba.

22. Yayin daya isa cikar ganiyar ƙarfinsa, shekara talatin sai muka bashi hukunci (wato hikima da fahinta a cikin addini, tun ba a aiko shi Annabi ba,) irin wannan sakamako muke sakawa masu kyautatawa.

وَرَٰوَدَتۡهُ ٱلَّتِي هُوَ فِي بَيۡتِهَا عَن نَّفۡسِهِۦ وَغَلَّقَتِ ٱلۡأَبۡوَٰبَ
وَقَالَتۡ هَيۡتَ لَكَۚ قَالَ مَعَاذَ ٱللَّهِۖ إِنَّهُۥ رَبِّيٓ أَحۡسَنَ
مَثۡوَايَۖ إِنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿23﴾ وَلَقَدۡ هَمَّتۡ بِهِۦۖ
وَهَمَّ بِهَا لَوۡلَآ أَن رَّءَا بُرۡهَٰنَ رَبِّهِۦۚ كَذَٰلِكَ لِنَصۡرِفَ
عَنۡهُ ٱلسُّوٓءَ وَٱلۡفَحۡشَآءَۚ إِنَّهُۥ مِنۡ عِبَادِنَا ٱلۡمُخۡلَصِينَ ﴿24﴾
وَٱسۡتَبَقَا ٱلۡبَابَ وَقَدَّتۡ قَمِيصَهُۥ مِن دُبُرٖ وَأَلۡفَيَا سَيِّدَهَا لَدَا ٱلۡبَابِۚ
قَالَتۡ مَا جَزَآءُ مَنۡ أَرَادَ بِأَهۡلِكَ سُوٓءًا إِلَّآ أَن يُسۡجَنَ
أَوۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ﴿25﴾ قَالَ هِيَ رَٰوَدَتۡنِي عَن نَّفۡسِيۚ وَشَهِدَ شَاهِدٞ
مِّنۡ أَهۡلِهَآ إِن كَانَ قَمِيصُهُۥ قُدَّ مِن قُبُلٖ فَصَدَقَتۡ وَهُوَ مِنَ ٱلۡكَٰذِبِينَ ﴿26﴾
وَإِن كَانَ قَمِيصُهُۥ قُدَّ مِن دُبُرٖ فَكَذَبَتۡ وَهُوَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿27﴾
فَلَمَّا رَءَا قَمِيصَهُۥ قُدَّ مِن دُبُرٖ قَالَ إِنَّهُۥ مِن كَيۡدِكُنَّۖ
إِنَّ كَيۡدَكُنَّ عَظِيمٞ ﴿28﴾ يُوسُفُ أَعۡرِضۡ عَنۡ هَٰذَاۚ
وَٱسۡتَغۡفِرِي لِذَنۢبِكِۖ إِنَّكِ كُنتِ مِنَ ٱلۡخَاطِـِٔينَ ﴿29﴾
وَقَالَ نِسۡوَةٞ فِي ٱلۡمَدِينَةِ ٱمۡرَأَتُ ٱلۡعَزِيزِ تُرَٰوِدُ فَتَىٰهَا عَن نَّفۡسِهِۦۖ
قَدۡ شَغَفَهَا حُبًّاۖ إِنَّا لَنَرَىٰهَا فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ﴿30﴾

23. wacce yake cikin dakinta, (Zaliha) ta neme shi bisa tilasarsa a kan ya sadu da ita, ta kulle ƙofofi, Tace dashi "Taho", yace "Allah ya kiyashe ni, haƙiƙa Ubangijina Tabaraka wata'ala, ya girmama makoma ta, haƙiƙa azzalumai bazasu tsira ba, (mazinata ko waɗansunsu".
24. Haƙiƙa tayi nufin saduwa dashi, yayi nufin Saduwa da ita ba don yaga burhamin Ubangijinsa ba (daya sadu da ita, Ibn Abbas yace, Annabi Yaƙubu Alaihissalamune ya bayyana gareshiya doki ƙirjinsa, sai sha'awarsa ta fice daga "yanyatsunsa,) kamar wancananka ne muka nuna masa wannan burhani, don mu juyar da aikin ha'inci da alfasha, zina, ga buran sa, haƙiƙa shi yana daga bayinnlu ababan tsarkakewa.
25. Suka girko aguje izuwa ƙofa, (yana nufin gudu, ita kuma tana nufin ta riƙe shi, ta kama tufansa, ta fisge shi izuwa gareta, ta keta rigarsa da ga baya,) suka Sami shugabanta, (wato mijinta,) nan ga ƙofar gida, (ta tsarkake kanta, sannan) tace, ba wani abin sakamakon wanda yanufi zina da iyalinka sai a ɗaure shi, ko azaba mai raɗaɗi (a doke shi".)
26. Annabi Yusufu (Alaihissalamu) yace, (yana mai kubutar da kansa,) "ITace ta neme ni bisa tilashina, "wani shaidaya shaida daga mutanenta, (ɗan amminta, yana cikin gunya,) yace, "Idan rigarsa an ketata daga gaba, to, ta gasgata shi yana daga cikin marasa gaskiya".
27. "Idan kuwa an ketata daga baya, to, tayi ƙarya, shi yana daga cikin masu gaskiya".
28. Yayin da mijinta yaga rigarsa an ketata daga baya, sai yace, "Haƙiƙa wannan magana (MAJAZA'U MAN ARADA) yana daga kaidinku ne, haƙiƙa kaidinku (ku mata) mai girma ne.
29. Sannan yace, "Ya Yusufu, kauda kanka ga buran wannan al'amari (kadaka gaya wa kowa,) dan kada ya daidaita, ke kuma Zaliha nemi gafara ga zunubinki, haƙiƙa ke kin kasance daga masu kuskure".

(YADUWAR LABARI A CIKIN GARI DA ABINDA YA BIYO WANNAN)

30. Sai (labarin ya bulla,) mataye a cikin birnin Misra suka dinga cewa, "Matar Ma'ajin Misra tana neman yaronta, ta tilashinsa, haƙiƙa ya lullubeta a soyayya, lalle mu, muna ganinta a cikin kuskure mabayyani".

فَلَمَّا سَمِعَتْ بِمَكْرِهِنَّ أَرْسَلَتْ إِلَيْهِنَّ وَأَعْتَدَتْ لَهُنَّ مُتَّكَأً وَءَاتَتْ كُلَّ
وَاحِدَةٍ مِّنْهُنَّ سِكِّينًا وَقَالَتُ اخْرُجْ عَلَيْهِنَّ فَلَمَّا رَأَيْنَهُ أَكْبَرْنَهُ وَقَطَّعْنَ
أَيْدِيَهُنَّ وَقُلْنَ حَاشَ لِلَّهِ مَا هَٰذَا بَشَرًا إِنْ هَٰذَا إِلَّا مَلَكٌ كَرِيمٌ ﴿31﴾
قَالَتْ فَذَٰلِكُنَّ الَّذِي لُمْتُنَّنِي فِيهِ وَلَقَدْ رَاوَدتُّهُ عَن نَّفْسِهِ فَاسْتَعْصَمَ
وَلَئِن لَّمْ يَفْعَلْ مَا ءَامُرُهُ لَيُسْجَنَنَّ وَلَيَكُونًا مِّنَ الصَّاغِرِينَ ﴿32﴾
* قَالَ رَبِّ السِّجْنُ أَحَبُّ إِلَيَّ مِمَّا يَدْعُونَنِي إِلَيْهِ وَإِلَّا تَصْرِفْ ربع
عَنِّي كَيْدَهُنَّ أَصْبُ إِلَيْهِنَّ وَأَكُن مِّنَ الْجَاهِلِينَ ﴿33﴾
فَاسْتَجَابَ لَهُ رَبُّهُ فَصَرَفَ عَنْهُ كَيْدَهُنَّ إِنَّهُ هُوَ السَّمِيعُ
الْعَلِيمُ ﴿34﴾ ثُمَّ بَدَا لَهُم مِّنۢ بَعْدِ مَا رَأَوُا الْآيَاتِ لَيَسْجُنُنَّهُ
حَتَّىٰ حِينٍ ﴿35﴾ وَدَخَلَ مَعَهُ السِّجْنَ فَتَيَانِ قَالَ أَحَدُهُمَا
إِنِّي أَرَانِي أَعْصِرُ خَمْرًا وَقَالَ الْآخَرُ إِنِّي أَرَانِي أَحْمِلُ فَوْقَ رَأْسِي
خُبْزًا تَأْكُلُ الطَّيْرُ مِنْهُ نَبِّئْنَا بِتَأْوِيلِهِ إِنَّا نَرَاكَ مِنَ الْمُحْسِنِينَ ﴿36﴾
قَالَ لَا يَأْتِيكُمَا طَعَامٌ تُرْزَقَانِهِ إِلَّا نَبَّأْتُكُمَا بِتَأْوِيلِهِ
قَبْلَ أَن يَأْتِيَكُمَا ذَٰلِكُمَا مِمَّا عَلَّمَنِي رَبِّي إِنِّي تَرَكْتُ
مِلَّةَ قَوْمٍ لَّا يُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ وَهُم بِالْآخِرَةِ هُمْ كَافِرُونَ ﴿37﴾

31. Yayin data ji sunayi mata giba, saita aika izuwa garesu, ta tanaji abinci, (Wanda, ake yanka shi da wuka wato, lemo,) ta ba kowace ɗaya daga garesu wuka, Tace (da Annabi Yusufu Alai-hissalamu) fito a kansu, ayayin da suka gan shi, sai suka girmama shi, suka yanyanke "yan yatsunsu, da wuƙaƙe basujizafi ba, saboda zuciyar su tazaru da Annabi Yusufu Sukace, "subuha-nallahi, wannan ai (annabi Yusufu Alaihissalam) bai kasance mutum ba, wannan bai kasance ba illa Mala'ika maigirma, (saboda abinda yake gareshi na daga kyau wanda baya kasancewa ga ɗan taliki ga al'ada, saboda shi an bashi rabin kyau) [1]

32. Matar Ma'ajin Misra Zaliha saitace, (yayin data ga abinda ya same su,) wancananku shine abinda kuke zargina a cikinsa, to, haƙiƙa na neme shi ga tilashinsa, saiya hanu, Wallahi in bai aikata abinda nake nufi dashi ba lalle za a daure shi a kurkuku, lalle zai kasance daga cikin wulaƙantattu. (Sai sukace dashi bi uwar (ɗakinka.)

33. Yace, "Ubangijina kurkuku shine yafi soyuwa izuwa gare ni da abinda suke kirana iziwa gareshi, idan baka juyar da kaidunsu ga barina ba, na karkata izuwa garesu, na kasance daga masu laifi (ma'ana kiyaye ni daga kaidunsu".)

34. Ubangijinsa ya amsa masa (addu'arsa,) saiya juyar da kai dunsu ga buransa, haƙiƙa Ubangiji shine mai jin (abinda ake faɗa ko ake aikatawa,) masani (da abinda ake faɗa ko aikatawa.)

35. Sannan ya bayyana a garesu (bayan sun ga alamomi na kubutarsa,) cewa lalle su ƙsaie shi, har izuwa wani lokaci, (wanda kwarmaton mutane zai yanke a cikinsa, to, sai aka tsare shi.)

(ANNABI YUSUFU ALAIHISSALAM A KURKUKU)

36. Samari guda biyu suka shiga kurkuku tare dashi, (yara ne guda biyu na Sarkin Misra, (ɗayansu, mai sha dashigiya ɗayansu mai bashi abinci, mai sha dashi, shine sarhamu, mai bada abinci Barhamu, sai suka gan shi yana fassara mafarki, sukace lalle mu gwadashi, ɗayansu yace, wato mai shayarwa, haƙiƙa ni na ganni ina nannagar inabi, ɗayan mai bada abinci yace, haƙiƙa ni na ga ina ɗauke da gurasa a bisa kaina, tsintsaye suna ci daga gurasar,) bamu labarin fassarar wannan mafarki, haƙiƙa mu muna ganinka kana daga cikin gwanaye, da fassarar mafarki (sai yace dasu lalle na san ilimin mafarki.)

(ANNABI YUSUFU YA FARA KIRA IZUWA ALLAH YANA FARKON BALIGI)

37. Abinci da aka azurta muku shi a cikin mafarkinku bazaizo muku ba face na baku labari da fassararsa a faɗake, tun kafin fassarar tazo muku, wancananku yana daga abinda Ubangijina yasanar da ni, (akwai kwaɗaitarwa a cikin imaninsu a wannan magana, sannan ya karfafi maganar da faɗinsa,) haƙiƙa ni na bar addinin mutanen da basu bada gaskiya da Allah ba, su sun kafirce da ranar Lahira.

1) a cikin hadisi sahihi.

وَاتَّبَعْتُ مِلَّةَ ءَابَآءِيَ إِبْرَٰهِيمَ وَإِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ مَا كَانَ
لَنَا أَن نُّشْرِكَ بِاللَّهِ مِن شَيْءٍ ذَٰلِكَ مِن فَضْلِ اللَّهِ عَلَيْنَا
وَعَلَى النَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ النَّاسِ لَا يَشْكُرُونَ (38)
يَٰصَٰحِبَيِ السِّجْنِ ءَآرْبَابٌ مُّتَفَرِّقُونَ خَيْرٌ اَمِ اللَّهُ الْوَٰحِدُ
الْقَهَّارُ (39) مَا تَعْبُدُونَ مِن دُونِهِۦٓ إِلَّآ أَسْمَآءً سَمَّيْتُمُوهَآ أَنتُمْ
وَءَابَآؤُكُم مَّآ أَنزَلَ اللَّهُ بِهَا مِن سُلْطَٰنٍ اِنِ الْحُكْمُ إِلَّا لِلَّهِ أَمَرَ
أَلَّا تَعْبُدُوٓاْ إِلَّآ إِيَّاهُ ذَٰلِكَ الدِّينُ الْقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ النَّاسِ
لَا يَعْلَمُونَ (40) يَٰصَٰحِبَيِ السِّجْنِ أَمَّآ أَحَدُكُمَا فَيَسْقِي رَبَّهُۥ خَمْرًا
وَأَمَّا الْأٓخَرُ فَيُصْلَبُ فَتَأْكُلُ الطَّيْرُ مِن رَّأْسِهِۦ قُضِيَ الْأَمْرُ الَّذِي
فِيهِ تَسْتَفْتِيَٰنِ (41) وَقَالَ لِلَّذِي ظَنَّ أَنَّهُۥ نَاجٍ مِّنْهُمَا
اذْكُرْنِي عِندَ رَبِّكَ فَأَنسَٰهُ الشَّيْطَٰنُ ذِكْرَ رَبِّهِۦ فَلَبِثَ
فِي السِّجْنِ بِضْعَ سِنِينَ (42) * وَقَالَ الْمَلِكُ إِنِّيَ أَرَىٰ سَبْعَ ثمن
بَقَرَٰتٍ سِمَانٍ يَأْكُلُهُنَّ سَبْعٌ عِجَافٌ وَسَبْعَ
سُنۢبُلَٰتٍ خُضْرٍ وَأُخَرَ يَابِسَٰتٍ يَٰٓأَيُّهَا الْمَلَأُ أَفْتُونِي
فِي رُءْيَايَ إِن كُنتُمْ لِلرُّءْيَا تَعْبُرُونَ (43)

38. Na bi addinin iyayena Annabi Ibrahim da Annabi Ishaƙa da Annabi Yaƙuba(alaihimussalam,) bai kamata garemu mu shirkanta wani abu da Allah ba, (saboda mu Allah ya azurta mu da (Ismah) [1] wancananka (tauhidi) yana daga falalar Allah garemu da kuma mutane. Yawaicin mutane basa gode wa Allah.
39. (Sannan Yakumrutada kiransu izuwa imani yace,) "Ya abokaina (na zaman kurkuku, yanzu iyayen giji daban daban su sukafi ko kuwa Allah maɗayancin sarki, mai yawan rinjaye?
40. Ba kwa bautawa bashi ba sai sunannaki da kuka ambaceta (gumaka), kuda iyayenku, Allah bai saukar da hujja ga bautar ta ba, hukunci bai kasance ba sai ga Allah shi kaɗai, yayi umarni kadaku ,bautawa kowa sai shi, wannan tauhidi shine addini na totar, sai dai yawaicin mutane basu sani ba.

(FASSARAR ANNABI YUSUFU ALAIHISSALAM GA MAFARKIN ABOKANSA SU BIYU)

41. "Ya abokaina biyu na cikin kurkuku, amma ɗayanku (shine Sarhamu, mai shayarwa, zai fita bayan kwana uku,) yaci gabada shayar da uban (ɗakinsa giya, (a bisa al'ada tasa.) Amma ɗayan, (Barhamu mai bada abinci) zai (fita bayan kwana uku) a tsire shi, tsintsaye su dinga tsatstsagar kansa, wannan shine fassarar mafarkinku, sai (sukace "Bamu ga komai ba, sai yace,) "Ai an gama hukuncin abinda kuke tambayona (a cikinsa, kun gasgata a ciki ko kun yi ƙarya".)
42. Ya faɗa ga wanda ya tabbata shi mai tsira ne daga cikinsu, (shine mai shayarwa,) ambace ni nan ga shugabanka, (kace dashi, "Akwai wani yaro da aka tsare shi don zalunci a kurkuku", sai yafita,) sai shaiɗan ya mantar dashi, ambaton Annabi Yusufu (Alaihissalamu) nan ga uban ɗakinsa, sai Annabi Yusufu (Alaihissalamu) ya zauna a cikin kurkuku tsirarin shekam, (shekara bakwai muddar zaman Annabi Ayuba Alaihissalam cikn bala'i.)

(FASSARAR ANNABI YUSUFU ALAIHISSALAM GA MAFARKIN SARKIN MISRA)

43. Sarkin Misra (Rayyanu ɗan Walidu yace [2] "Ni na ga shanu guda bakwai masu kiba, shanu bakwai kanjamammu suna cinye su, da zangarnu bakwai kwarra da wadansu bakwai ƙeƙasassu ta lanyace kwarran nan Yaku wannan jama'a masu daraja, kuyi min fassara ta mafarkina, in kun kasance kuna fassara mafarki, to, ku fassara min ita".)

1) Hanuwa ga buian dukkan saɓo.
2) Lafazin "maliku" da kuma rayyanu dan walidu sun nuna cewa daular misra ta waccan lokacio balarabi, yace - Sanajiy -

قَالُوٓاْ أَضۡغَٰثُ أَحۡلَٰمٖۖ وَمَا نَحۡنُ بِتَأۡوِيلِ ٱلۡأَحۡلَٰمِ بِعَٰلِمِينَ ﴿٤٤﴾
وَقَالَ ٱلَّذِي نَجَا مِنۡهُمَا وَٱدَّكَرَ بَعۡدَ أُمَّةٍ أَنَا۠ أُنَبِّئُكُم بِتَأۡوِيلِهِۦ
فَأَرۡسِلُونِ ﴿٤٥﴾ يُوسُفُ أَيُّهَا ٱلصِّدِّيقُ أَفۡتِنَا فِي سَبۡعِ بَقَرَٰتٖ سِمَانٖ
يَأۡكُلُهُنَّ سَبۡعٌ عِجَافٞ وَسَبۡعِ سُنۢبُلَٰتٍ خُضۡرٖ وَأُخَرَ يَابِسَٰتٖ لَّعَلِّيٓ
أَرۡجِعُ إِلَى ٱلنَّاسِ لَعَلَّهُمۡ يَعۡلَمُونَ ﴿٤٦﴾ قَالَ تَزۡرَعُونَ سَبۡعَ سِنِينَ دَأَبٗا
فَمَا حَصَدتُّمۡ فَذَرُوهُ فِي سُنۢبُلِهِۦٓ إِلَّا قَلِيلٗا مِّمَّا تَأۡكُلُونَ ﴿٤٧﴾ ثُمَّ يَأۡتِي
مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ سَبۡعٞ شِدَادٞ يَأۡكُلۡنَ مَا قَدَّمۡتُمۡ لَهُنَّ إِلَّا قَلِيلٗا مِّمَّا
تُحۡصِنُونَ ﴿٤٨﴾ ثُمَّ يَأۡتِي مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ عَامٞ فِيهِ يُغَاثُ ٱلنَّاسُ وَفِيهِ
يَعۡصِرُونَ ﴿٤٩﴾ وَقَالَ ٱلۡمَلِكُ ٱئۡتُونِي بِهِۦۖ فَلَمَّا جَآءَهُ ٱلرَّسُولُ قَالَ ٱرۡجِعۡ
إِلَىٰ رَبِّكَ فَسۡـَٔلۡهُ مَا بَالُ ٱلنِّسۡوَةِ ٱلَّٰتِي قَطَّعۡنَ أَيۡدِيَهُنَّۚ
إِنَّ رَبِّي بِكَيۡدِهِنَّ عَلِيمٞ ﴿٥٠﴾ قَالَ مَا خَطۡبُكُنَّ إِذۡ رَٰوَدتُّنَّ يُوسُفَ
عَن نَّفۡسِهِۦۚ قُلۡنَ حَٰشَ لِلَّهِ مَا عَلِمۡنَا عَلَيۡهِ مِن سُوٓءٖۚ
قَالَتِ ٱمۡرَأَتُ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡـَٰٔنَ حَصۡحَصَ ٱلۡحَقُّ أَنَا۠ رَٰوَدتُّهُۥ
عَن نَّفۡسِهِۦ وَإِنَّهُۥ لَمِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿٥١﴾ ذَٰلِكَ لِيَعۡلَمَ أَنِّي
لَمۡ أَخُنۡهُ بِٱلۡغَيۡبِ وَأَنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي كَيۡدَ ٱلۡخَآئِنِينَ ﴿٥٢﴾

44. Sukace, "Wađannan Rikice -Rikiceane na mafarki, mu bamu kasance masana fassarar mafarkemafarke ba".
45. Wanda ya tsira daga wađancan samari guda biyu, (wato mai shayarwa,) sai yace, ya tuna bayan lokaci mai tsawo, ya tuna halin Annabi Yusufu, ni zan zo mukuda fassarar mafarkin. Ku aike ni, sai suka aike shi, sai yazowa Annabi Yusufu yace;)
46. "Ya yusufu, ya kai mai yawan gaskiya, yi mana fatawa a cikin shanu guda bakwai masu ƙiba, guda bakwai ƙanjamammu suna cinye su, da zangannu guda bakwai kwarra da wađansu ƙeƙasassu, saboda in koma zuwa mutane, (sarki da sahabbansa) don wata kila sa san fassarar wannan mafarki".
47. Yace, "Sai kuyi shuka shekara bakwai a jere, (shine fassarar bakwai masu ƙiba,) abinda kuka girbe ku bar shi a cikin zangarniyarsa (don kada ya baci,) sai kađan daga abinda zaKuci ku cashe shi
48. "Sannan bayan wannan bakwai masu ni'ima shekaru bakwai zasuzo masu tsanani, zasu cinye abinda kuka gabatar musu na daga ƙwaya abar shekawa a cikin shekaru na ni'ima, (shine fassarar bakwai kanjamammu,) sai ƙadan daga abinda kuke ɓoyewa.
49. "Bayan wancananka shekarun fari, shekara zai zodaza a taimaki mutane da ruwa a cikinsa, a cikinsa zasu dinga nannagar inabi da waninsa, (saboda damina tayi albarka".)

(NEMAN MULKI GA ANNABI YUSUFU ALAIHISSALAMU DA HIKIMAR ANNABI YUSUFU ALAIHISSALAMU)

50. Sai sarkin ya fađa (yayin da ja-kada ya zo ya fađa masa fassarar mafarkinsa,) kuzo min dashi, (wato mai fassarar nan,) yayin da jakadan nan yazowa Annabi Yusufu (Alaihissalam ya nemi su fita, sai yace masa,yana mai nufin bayyana kubutarsa,) koma izuwa uban dakinka, ka tambaye shi, ya tambaya meye halin matayen da suka yanyanke hannuwansu, haƙiƙa Ubangijina masanine da kaidunsu, (yakoma ya baiwa sarki labarinsu
51. Saiya tara su yace meye sha'aninku, lokacin da kuka nemi Annabi Yusufu ga tilashin kansa, (kun sami karkata daga gareshi izuwa gareku, sukace Allah ya kiyashemu, bamu san wani mummunan abu a gareshi ba,) sai matar Ma'ajin Misra tace, a yanzu gaskiya ta tambaya, ni ce na neme shi bisa tilashin kansa, haƙiƙa shi yana daga magasgata (a cikin fađinsa iTace ta neme ni a bisa tilashina, to, sai aka baiwa Annabi Yusufu labari da wannan, sai yace-)
52. Wancananka neman kubuta saboda Ma'ajin Misra yasan cewa ni ban ha'ince shi cikin iyalinsa a bayan idonsa ba, haƙiƙa Allah ɓaya shiriyar kaidun masu cin amana.

(TAWALITUN ANNABI YUSUFU ALAIHISSALAMU DA RASHIN YARDA DA KANSA)

حزب

۞ وَمَا أُبَرِّئُ نَفْسِيٓ إِنَّ ٱلنَّفْسَ لَأَمَّارَةُۢ بِٱلسُّوٓءِ إِلَّا مَا رَحِمَ رَبِّيٓ إِنَّ رَبِّي
غَفُورٞ رَّحِيمٞ ﴿53﴾ وَقَالَ ٱلْمَلِكُ ٱئْتُونِي بِهِۦٓ أَسْتَخْلِصْهُ لِنَفْسِي
فَلَمَّا كَلَّمَهُۥ قَالَ إِنَّكَ ٱلْيَوْمَ لَدَيْنَا مَكِينٌ أَمِينٞ ﴿54﴾ قَالَ ٱجْعَلْنِي
عَلَىٰ خَزَآئِنِ ٱلْأَرْضِ إِنِّي حَفِيظٌ عَلِيمٞ ﴿55﴾ وَكَذَٰلِكَ مَكَّنَّا لِيُوسُفَ
فِي ٱلْأَرْضِ يَتَبَوَّأُ مِنْهَا حَيْثُ يَشَآءُ نُصِيبُ بِرَحْمَتِنَا مَن
نَّشَآءُ وَلَا نُضِيعُ أَجْرَ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿56﴾ وَلَأَجْرُ ٱلْأٓخِرَةِ خَيْرٞ
لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَكَانُواْ يَتَّقُونَ ﴿57﴾ وَجَآءَ إِخْوَةُ يُوسُفَ
فَدَخَلُواْ عَلَيْهِ فَعَرَفَهُمْ وَهُمْ لَهُۥ مُنكِرُونَ ﴿58﴾ وَلَمَّا جَهَّزَهُم
بِجَهَازِهِمْ قَالَ ٱئْتُونِي بِأَخٖ لَّكُم مِّنْ أَبِيكُمْۚ أَلَا تَرَوْنَ
أَنِّيٓ أُوفِي ٱلْكَيْلَ وَأَنَا۠ خَيْرُ ٱلْمُنزِلِينَ ﴿59﴾ فَإِن لَّمْ تَأْتُونِي بِهِۦ فَلَا كَيْلَ
لَكُمْ عِندِي وَلَا تَقْرَبُونِ ﴿60﴾ قَالُواْ سَنُرَٰوِدُ عَنْهُ أَبَاهُ وَإِنَّا
لَفَٰعِلُونَ ﴿61﴾ وَقَالَ لِفِتْيَٰنِهِ ٱجْعَلُواْ بِضَٰعَتَهُمْ فِي رِحَالِهِمْ
لَعَلَّهُمْ يَعْرِفُونَهَآ إِذَا ٱنقَلَبُوٓاْ إِلَىٰٓ أَهْلِهِمْ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿62﴾
فَلَمَّا رَجَعُوٓاْ إِلَىٰٓ أَبِيهِمْ قَالُواْ يَٰٓأَبَانَا مُنِعَ مِنَّا ٱلْكَيْلُ
فَأَرْسِلْ مَعَنَآ أَخَانَا نَكْتَلْ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ ﴿63﴾

53. Yace, "Bana kubutar da kaina daga tuntube, haƙiƙa raguwar zuciya mai yawan umarni ce da mummunan aiki, sai wanda Ubangiji yajiƙansa, ya bashi (Ismah) wato kiyayewa daga sabo, da zummar annabci, ko Mala'ikanci,) haƙiƙa Ubangij na mai yawan garara ne mai Jinkai.
54. Sarkin Misra yace, kuzo min dashi, in maidashi ɗan morina, (sai jakada ya zo masa yace, sai ka amsawa sarki, saiya tashi yayi bankwana da "yan kurkuku, yayi musu kyakkyawar addu'a ya ɗaura tufafi kyawawa, ya shiga gareshi,) yayin dayayi zance dashi sai yace, "Haƙiƙa kai, a yau matabbacin da raja ne garemu, amintacce", (to, me kake ganin zamu aikata, sai yacc tara abinci kayi shuka mai yawa a cikin wannan shekaru na fari, ka ɓoye abinci a cikin zangarniyarsa, mutane zasuzo gareka don neman abinci daga gareka, sai yace waye zai tsaya min da wannan.)
55. Sai (Annabi Yusufu Alaihissalamu) yace sanya ni bisa taskokin ƙasar Misra, haƙiƙa ni mai kiyayewa ne masani ne, na iya rubutu da lissafi da sauran irinsu.
56. Kamar yadda mukayi ni ima gareshi da kubuta daga kurkuku, hakana muka bunƙasar da Annabi Yusufu (Alaihissalamu) a kasar Misra, yana sauka in dayaga dama a gareta, (bayan kunci da tsarewa a cikin wannan kissa cewa sarki ya daura masa kambi da kwandage, Ya sanyashi matsayin Ma'ajin Misra, bayan ya tube shiya aura masa matarsa Zaliha bayan mutuwarsa, ya same ta "ya, ta haifa masa "ya"ya biyu maza da mace Rahamatu, ya tsayar da adalci a Misra, sarakuna suka ranƙasa masa,) Muna samun wanda muka ga dama dajinkan-mu, Barna tozarta ladan masu kyakkyawan aiki.
57. Lalle ladan Lahira shine yafi na duniyaga waɗanda suka bada gaskiya suke jin tsoron Allah, (shekamn fari suka shigo ya sami ƙasar kan'ana da Sham.)

("YAN UWAN ANNABI YUSUFU SUNA SAYEN ABINCI DAGA GARESHI)

58. "YAn'uwan Annabi Yusufu sukazo (sai Bunyaminu saboda neman abinci, yayin da sukaji Ma'ajin Misra yana bada abinci da tamaninsa,) suka shigo gareshi saiya shaidasu, amma su basu san shine ba, (saboda nisan zamaninsu dashi da zaton halakarsa. sukayi zance dashi dayaren Abraniya yace, Me ya kawo ku kasata, sukace neman abinci, yace watakila "yan leken asirin ƙasa ne, sukace Allah ya kiyashemu, yace daga ina kuke, sukace daga kasar kan'ana, (wato Nabulus.) Ubanmu Yaƙubu Annabin Allah ne, yace yana da waɗansu "ya" ya ban da ku, sukace na'am, mu goma sha biyu ne, ƙaraminmu ya nausa duniya, ubanmu yafi sonsa, mun bar masa shaƙiƙinsa don yasanyaya dashi, sai yace a saukar dasu a girmama su.)
59. Yayin daya shiryasu dashirinsu, ya cika musu awo, sai yace, "kuzo min da ɗan uwanku Bunyaminu don in san gaskiyarku a cikin abinda kuka faca,) ba kvva ganin haƙiƙa ni ina cika awo, kuma na fi dukkan masu saukar da baƙi.
60. To, in bakuzo min dashi ba, to, fa bakuda awo guna, kadaku ,kusance ni".
61. Sukace, "Da sannu zamuyi ƙoƙarin karɓo shi daga ubansa, haƙiƙa mu masu aikata haka ne".
62. Yace da samarinsa, ku sanya jakar kuɗinsu a cikin burgangaminsu, ko sa ganta idan sun koma izuwa iyalinsa idan suka zazzage burgangaminsu, ko sa komo izuwa garemu, (saboda haka haƙiƙa bazasu iya halarta riƙc ta ba.)

("YAN'UWAN ANNABI YUSUFU TAREDA BABANSU BAYAN KOMOWAR SU DAGA GARESHI)

63. Yayin da suka koma izuwa babansu, sai Sukace, "Ya babanmu! an hana mana awo, sai in mun kai masa dan'uwanmu, barshi tareda mu mu auno abinci, haƙiƙa mu, masu kiyayewa ne gareshi".

قَالَ هَلْ ءَامَنُكُمْ عَلَيْهِ إِلَّا كَمَا أَمِنتُكُمْ عَلَىٰٓ أَخِيهِ
مِن قَبْلُ فَٱللَّهُ خَيْرٌ حِفْظًا وَهُوَ أَرْحَمُ ٱلرَّٰحِمِينَ ﴿64﴾
وَلَمَّا فَتَحُوا۟ مَتَٰعَهُمْ وَجَدُوا۟ بِضَٰعَتَهُمْ رُدَّتْ إِلَيْهِمْ قَالُوا۟ يَٰٓأَبَانَا
مَا نَبْغِى هَٰذِهِۦ بِضَٰعَتُنَا رُدَّتْ إِلَيْنَا وَنَمِيرُ أَهْلَنَا وَنَحْفَظُ أَخَانَا
وَنَزْدَادُ كَيْلَ بَعِيرٍ ذَٰلِكَ كَيْلٌ يَسِيرٌ ﴿65﴾ قَالَ لَنْ
أُرْسِلَهُۥ مَعَكُمْ حَتَّىٰ تُؤْتُونِ مَوْثِقًا مِّنَ ٱللَّهِ لَتَأْتُنَّنِى بِهِۦٓ
إِلَّآ أَن يُحَاطَ بِكُمْ فَلَمَّآ ءَاتَوْهُ مَوْثِقَهُمْ قَالَ ٱللَّهُ عَلَىٰ مَا نَقُولُ
وَكِيلٌ ﴿66﴾ * وَقَالَ يَٰبَنِىَّ لَا تَدْخُلُوا۟ مِنۢ بَابٍ وَٰحِدٍ وَٱدْخُلُوا۟ ثمن
مِنْ أَبْوَٰبٍ مُّتَفَرِّقَةٍ وَمَآ أُغْنِى عَنكُم مِّنَ ٱللَّهِ مِن شَىْءٍ
إِنِ ٱلْحُكْمُ إِلَّا لِلَّهِ عَلَيْهِ تَوَكَّلْتُ وَعَلَيْهِ فَلْيَتَوَكَّلِ ٱلْمُتَوَكِّلُونَ ﴿67﴾
وَلَمَّا دَخَلُوا۟ مِنْ حَيْثُ أَمَرَهُمْ أَبُوهُم مَّا كَانَ يُغْنِى
عَنْهُم مِّنَ ٱللَّهِ مِن شَىْءٍ إِلَّا حَاجَةً فِى نَفْسِ يَعْقُوبَ قَضَىٰهَا
وَإِنَّهُۥ لَذُو عِلْمٍ لِّمَا عَلَّمْنَٰهُ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿68﴾
وَلَمَّا دَخَلُوا۟ عَلَىٰ يُوسُفَ ءَاوَىٰٓ إِلَيْهِ أَخَاهُ قَالَ إِنِّىٓ
أَنَا۠ أَخُوكَ فَلَا تَبْتَئِسْ بِمَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿69﴾

64. Yace, "Ni ban aminceku a kansa ba, sai kamar yaddana aminceku a bisa dan'uwansa Annabi Yusufu tun gaba, (alhali kuma kun yi masa abinda kukayi masa,) Allah shine mafi kiwo, shine mafi jinƙan masu jinƙai, (ina ƙauna yayi min baiwa da kiyaye shi".)
65. A yayin da suka buɗe tarkacensu, sai suka sami jakar kuɗinsu an mayar izuwa garesu, Sukace, "Ya babanmu me muke nema na daga girmama wan sarki garemu fiyeda wannan, wannan kuɗinmune an komo mana dasu izuwa garemu, zamu kuma ci da iyalinmu, zamu kiyaye ɗan'uwanmu, zamu ɗaɗa awon raƙumi guda, wancananka awo ne mai sauki (wurin sarki saboda karimcinsa".)
66. Yace, "Ni bazan sake shi taredaku ,ba sai kun bani alƙawari daga Allah (shine ku rantse lalle zakuzo min dashi,) sai ko in an karɓi ranku," (shine kun mutu ko an rinjaye ku, suka amsa wannn,) yayin da suka bashi alƙawarinsu da wannan, sai yace, "Allah shine shaida a bisa abinda muke faɗa (mu da ku, saiya basu shi.)

(ANNABI YAKUBU ALAIHISSALAM YANAYI WA "YA"YANSA WASIYYA MASU ZUWA MISRA, WANDA YAKUNSHI CEWA KAMBIN BAKA GASKIYA NE)

67. "Yaku "ya"yana kadaku ,shiga Misra ta ƙofa ɗaya, ku shiga ta ƙofofi daban daban don (kada idaniya ta same ku,) ni bazan wadatar mukuda komai gun Allah ba, hukunci bai kasance ba sai ga Allah shi kaɗai, a gareshi na dogara a gareshi masu dogaro su dogara".
68. Yayin da suka shiga ta inda ubansu ya umarce su dabandaban bai kasance bazai ije komai ga buransu daga hukuncin Allah, sai dai bukaTace a zuciyar Annabi Yaƙubu ya biyata (wato ije kambin baka ga buran "ya"yansa don tausayinsu,) haƙiƙa, shi, ma'abucin ilimi ne ga abinda muka sanar dashi, sai dai yawaicin mutane basu san ilhamin Allah ga tsarkakansa ba.)

(ANNABI YUSUFU ALAIHISSALAM YANA SANAR DA KANSA GA DAN UWANSA BINYAMINU YANA DAB-ARARWANZAR DASHI GUNSA)

69. Yayin da suka shiga zuwa Annabi Yusufu saiya tattara dan uwansa izuwa gareshi, yace "Haƙiƙa nine ɗan uwanka, kada kayi baƙin ciki da abinda suka kasance suna aikatawa (na hassada", (ya umarce shi kada ya basu labari, suka game kai a kan cewa da sannu zaiyi dabarar wanzar dashi nan gareshi.)

فَلَمَّا جَهَّزَهُم بِجَهَازِهِمْ جَعَلَ اَ۬لسِّقَايَةَ فِے رَحْلِ أَخِيهِ
ثُمَّ أَذَّنَ مُؤَذِّنٌ أَيَّتُهَا اَ۬لْعِيرُ إِنَّكُمْ لَسَٰرِقُونَ ﴿70﴾ قَالُواْ وَأَقْبَلُواْ
عَلَيْهِم مَّاذَا تَفْقِدُونَ ﴿71﴾ قَالُواْ نَفْقِدُ صُوَاعَ اَ۬لْمَلِكِ وَلِمَن
جَآءَ بِهِۦ حِمْلُ بَعِيرٍ وَأَنَا بِهِۦ زَعِيمٌ ﴿72﴾ قَالُواْ تَاللَّهِ لَقَدْ عَلِمْتُم
مَّا جِئْنَا لِنُفْسِدَ فِے اِ۬لْأَرْضِ وَمَا كُنَّا سَٰرِقِينَ ﴿73﴾ قَالُواْ
فَمَا جَزَٰٓؤُهُۥ إِن كُنتُمْ كَٰذِبِينَ ﴿74﴾ قَالُواْ جَزَٰٓؤُهُۥ مَن وُجِدَ
فِے رَحْلِهِۦ فَهُوَ جَزَٰٓؤُهُۥ كَذَٰلِكَ نَجْزِے اِ۬لظَّٰلِمِينَ ﴿75﴾
فَبَدَأَ بِأَوْعِيَتِهِمْ قَبْلَ وِعَآءِ أَخِيهِ ثُمَّ اَ۪سْتَخْرَجَهَا مِن
وِعَآءِ أَخِيهِ كَذَٰلِكَ كِدْنَا لِيُوسُفَ مَا كَانَ
لِيَأْخُذَ أَخَاهُ فِے دِينِ اِ۬لْمَلِكِ إِلَّآ أَن يَشَآءَ اَ۬للَّهُ نَرْفَعُ
دَرَجَٰتٍ مَّن نَّشَآءُ وَفَوْقَ كُلِّ ذِے عِلْمٍ عَلِيمٌ ﴿76﴾ * قَالُواْ إِن
يَسْرِقْ فَقَدْ سَرَقَ أَخٌ لَّهُۥ مِن قَبْلُ فَأَسَرَّهَا يُوسُفُ
فِے نَفْسِهِۦ وَلَمْ يُبْدِهَا لَهُمْ قَالَ أَنتُمْ شَرٌّ مَّكَاناً وَاللَّهُ أَعْلَمُ
بِمَا تَصِفُونَ ﴿77﴾ قَالُواْ يَٰٓأَيُّهَا اَ۬لْعَزِيزُ إِنَّ لَهُۥ أَباً شَيْخاً كَبِيراً
فَخُذْ أَحَدَنَا مَكَانَهُۥ إِنَّا نَرَيٰكَ مِنَ اَ۬لْمُحْسِنِينَ ﴿78﴾

ربع

70. Yayin daya shirya su da tarkacensu, sai yasanya ma'auni a cikin kayan ɗan uwansa, sai mai kira yayi kira (bayan sun rabu daga majalisar Annabi Yusufu,) "Yaku waɗannan "yan kwarami haƙiƙa ku ɓarayi ne".
71. Sukace, alhali sun gabato a garesu, "Me kuka rasa?"
72. Sukace, ":Mun rasa ma'aunin sarki, wanda yazo dashi yana da kayan raƙumi na abinci, ni malamin ci ne dashi."
73. Sukace, mana ki, Allah, haƙiƙa kun sani bamu zo don mu yi barna a cikin ƙasa ba, bamu kasance ɓarayi ba, (bamu taɓa sata badaɗai.)
74. shi mai kiran nan da abokansa Sukace, "Meye sakamakon ɓarawon nan in kun kasance maƙaryata (a cikin faɗinku, bamu kasance ɓarayi ba.)
75. sai Sukace, "Sakamakonsa wanda aka samu a kayansa, sai a bautar dashi,) to, shi ɓarawon nan shine sakamakon abinda aka sace", (Wanda kuma wan-nan shine al'adar ali -Yaƙuba,) kamar wancananka sakamako muke sakawa ɓarayi (da makamantansu, sai aka juyar dasu izuwa Annabi Yusufu saboda abinciki kayayyakinsu.)
76. Aka fara da kayayyakinsu (aka binciketa gaban ta ɗan'uwansa (don kawar da hankali,) sannan yafitar da ma'aunin nan daga kayan ɗan' uwansa. Tamfar wancananka shiri, muka koyawa Annabi Yusufu wannan shiri, bai kasance zai kama ɗan'uwansa a cikin al'adar Sarkin Misra ba, (doirtin sakamakon sa nan ga Sarkin Misra shine duka da ninka abinda aka sata,) sai in Allah yanufi (kaɓo shi da hukuncin ubansu, ai bai sami ikon karɓo shi ba saida nufin Allah, daya kimsa masa tambayar "yan uwansa da amsawarsu da al'adarsu,)muna ɗaga darajojin waɗanda muka ga dama (da ilimi,) kowane masani akwai masani sama dashi (har dai ilimi ya tuƙe izuwa Allah.)

(ANSHESHENIYA TSAKANIN ANNABI YUSUFU DA"YAN UWANSA A KUMA TSAKANIN MAHAIFINSU YAƘUBU ALAIHIMUSSALAM)

77. Sukace, "Idan yayi sata, to hakika dan uwansa ya taɓa yin sata tun gabansa, (ya sace wani gunki na kakansa uban uwarsa, na zinare ya karairaya shi don kada ya bauta masa.)Sai Annabi Yusufu ya ɓoye wannan magana a cikin zuciyarsa, (bai bayyana wannan kalma garesu ba, wacce itace,) yace, "Kune mafi sharrin mazauni daga Yusufa da ɗan uwansa, (don kun sace ɗan uwanku li'abbi kun zalunce shi,) Allah ne masani da abinda kuke kwatantawa".
78. Sukace, "Ya wannan ma'aji, haƙiƙa buni yaminu yana da uba tsoho mai girma, (yana sonsa fiye da mu, yana sanyayawa dashi maimakon ɗansa daya ɓata,) sai ka riƙi dayanmu (maimakonsa,) haƙiƙa mu muna ganinka kana daga cikin masu ƙyakkyawan aiki".

قَالَ مَعَاذَ اللَّهِ أَن نَّأْخُذَ إِلَّا مَن وَجَدْنَا مَتَاعَنَا عِندَهُۥ
إِنَّا إِذًا لَّظَالِمُونَ ﴿79﴾ فَلَمَّا اسْتَيْـَٔسُوا مِنْهُ خَلَصُوا نَجِيًّا
قَالَ كَبِيرُهُمْ أَلَمْ تَعْلَمُوا أَنَّ أَبَاكُمْ قَدْ أَخَذَ عَلَيْكُم
مَّوْثِقًا مِّنَ اللَّهِ وَمِن قَبْلُ مَا فَرَّطتُّمْ فِي يُوسُفَ فَلَنْ أَبْرَحَ
الْأَرْضَ حَتَّىٰ يَأْذَنَ لِيَ أَبِيَ أَوْ يَحْكُمَ اللَّهُ لِي وَهُوَ خَيْرُ الْحَاكِمِينَ ﴿80﴾
ارْجِعُوا إِلَىٰ أَبِيكُمْ فَقُولُوا يَا أَبَانَا إِنَّ ابْنَكَ سَرَقَ
وَمَا شَهِدْنَا إِلَّا بِمَا عَلِمْنَا وَمَا كُنَّا لِلْغَيْبِ حَافِظِينَ ﴿81﴾
وَسْـَٔلِ الْقَرْيَةَ الَّتِي كُنَّا فِيهَا وَالْعِيرَ الَّتِي أَقْبَلْنَا فِيهَا
وَإِنَّا لَصَادِقُونَ ﴿82﴾ قَالَ بَلْ سَوَّلَتْ لَكُمْ أَنفُسُكُمْ
أَمْرًا فَصَبْرٌ جَمِيلٌ عَسَى اللَّهُ أَن يَأْتِيَنِي بِهِمْ جَمِيعًا
إِنَّهُۥ هُوَ الْعَلِيمُ الْحَكِيمُ ﴿83﴾ وَتَوَلَّىٰ عَنْهُمْ وَقَالَ يَا أَسَفَىٰ
عَلَىٰ يُوسُفَ وَابْيَضَّتْ عَيْنَاهُ مِنَ الْحُزْنِ فَهُوَ كَظِيمٌ ﴿84﴾
قَالُوا تَاللَّهِ تَفْتَؤُا تَذْكُرُ يُوسُفَ حَتَّىٰ تَكُونَ حَرَضًا
أَوْ تَكُونَ مِنَ الْهَالِكِينَ ﴿85﴾ قَالَ إِنَّمَا أَشْكُوا بَثِّيَ
وَحُزْنِيَ إِلَى اللَّهِ وَأَعْلَمُ مِنَ اللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿86﴾

79. Yace, "Allah ya kiyashe ni mu riƙa, sai wanda muka sami kayanmu gunsa, (bai ce wanda yayi sata ba don gudun ƙarya,) haƙiƙa mu, yayin nan muna daga cikin azzalumai (in mun riƙi waninsa.)

80. Yayin da suka ɗebe haso daga gareshi, sai suka koma waje ɗaya suna ganawa, babbansu a shekaru, (Raubilu, ko a wani ra'ayi Yahuza) yace, "Ai kun sani cewa ubanku ya riƙi alƙawari a kanku daga Allah a cikin ɗan'uwanku, da can kuma kun yi sakaci a cikin Yusufu, ni bazan bar ƙasar Misra ba, sai babana yayi min izini da komawa daga gareshi, ko Ubangiji yayi hukunci (a gareni da kuɓutar ɗan uwana,) shine mafi mahukunta iya hukunci.

81. "Ku koma izuwa ubanku, ku ce ya babanmu, haƙiƙa ɗanka yayi sata, bamu shaida ba sai abinda muka sani, bamu kasance masu kiyayewa gaibu ba.

(ZANCE DA SANDARARRU)

82. "Tambayi alƙarya wadda muka kasance a cikinta (wato Misra, wacce aka aiko su izuwa gareta, ka tambaye su,) da ayari, (wato sune "yan kwararo,) wacce muka gabato a cikinta (wato Kan'ana,) haƙiƙa mu magasgata ne (a cikin maganarmu, suka koma gareshi suka gaya masa haka",)

83. Yace, "Kai dai kawukanku ta kawata muku al'amari ne kuka aiwata shi, (ya tuhunce su saboda abinda ya rigaya na daga al'amarin Annabi Yusufu,) to, haKuri kyakkyawa shi ne haƙurina, ina ƙauna Ubangiji yazo min dasu, (Yusufu da ɗan uwarisa ya haɗa dasu) baki ɗaya, haƙiƙa Ubangiji shine masani (da halina gwani cikin (aikinsa".)

84. Ya juyaga buransu yace "Waiyo baƙin cikina a bisa Yusufu! idanuwansa guda biyu sukayi fari fat saboda kukansa (don baƙin ciki a kan Annabi Yusufu,) alhali shi yana mai haɗiye fishinsa.

85. Sukace, "Wo-ho-ho! Mun rantse da Allah bazaka gushe bakana ambaton Yusufu har ka zama mai sharafa, (saboda tsawon rashin lafiyarka,) ko ka zama daga matattu".

86. Yace (dasu) ni dai ina kai ƙarar baƙin cikina ne izuwa Allah, kuma ina sani daga Allah abinda baku sani ba, (na cewar mafarkin Annabi Yusufu gaskiya ne, shi rayayye ne".)

يَٰبَنِيَّ ٱذْهَبُواْ فَتَحَسَّسُواْ مِن يُوسُفَ وَأَخِيهِ وَلَا تَاْيْـَٔسُواْ مِن رَّوْحِ ٱللَّهِ
إِنَّهُۥ لَا يَاْيْـَٔسُ مِن رَّوْحِ ٱللَّهِ إِلَّا ٱلْقَوْمُ ٱلْكَٰفِرُونَ ﴿87﴾
۞ فَلَمَّا دَخَلُواْ عَلَيْهِ قَالُواْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلْعَزِيزُ مَسَّنَا
وَأَهْلَنَا ٱلضُّرُّ وَجِئْنَا بِبِضَٰعَةٍ مُّزْجَىٰةٍ فَأَوْفِ
لَنَا ٱلْكَيْلَ وَتَصَدَّقْ عَلَيْنَآ إِنَّ ٱللَّهَ يَجْزِي ٱلْمُتَصَدِّقِينَ ﴿88﴾
قَالَ هَلْ عَلِمْتُم مَّا فَعَلْتُم بِيُوسُفَ وَأَخِيهِ إِذْ
أَنتُمْ جَٰهِلُونَ ﴿89﴾ قَالُوٓاْ أَءِنَّكَ لَأَنتَ يُوسُفُ قَالَ أَنَا۠ يُوسُفُ
وَهَٰذَآ أَخِي قَدْ مَنَّ ٱللَّهُ عَلَيْنَآ إِنَّهُۥ مَن يَتَّقِ وَيَصْبِرْ
فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يُضِيعُ أَجْرَ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿90﴾ قَالُواْ تَٱللَّهِ
لَقَدْ ءَاثَرَكَ ٱللَّهُ عَلَيْنَا وَإِن كُنَّا لَخَٰطِـِٔينَ ﴿91﴾
قَالَ لَا تَثْرِيبَ عَلَيْكُمُ ٱلْيَوْمَ يَغْفِرُ ٱللَّهُ لَكُمْ وَهُوَ أَرْحَمُ
ٱلرَّٰحِمِينَ ﴿92﴾ ٱذْهَبُواْ بِقَمِيصِي هَٰذَا فَأَلْقُوهُ عَلَىٰ وَجْهِ أَبِي
يَأْتِ بَصِيرًا وَأْتُونِي بِأَهْلِكُمْ أَجْمَعِينَ ﴿93﴾ وَلَمَّا فَصَلَتِ
ٱلْعِيرُ قَالَ أَبُوهُمْ إِنِّي لَأَجِدُ رِيحَ يُوسُفَ لَوْلَآ أَن
تُفَنِّدُونِ ﴿94﴾ قَالُواْ تَٱللَّهِ إِنَّكَ لَفِي ضَلَٰلِكَ ٱلْقَدِيمِ ﴿95﴾

87. Sannan yace, "Yaku "ya" yana, ku tafi ku je ku samo min labarin Annabi Yusufa da ɗan uwansa, kadaku ,debe haso daga rahamar Ubangiji, ba mai ɗebe haso daga rahamar Allah sai mutane kafirai". (Sai suka tafi Misra zuwa ga Annabi Yusufa.)

(YAYUWAR "YAN UWAN ANNABI YUSUFU GARESHI DA FURUCINSU DA LAIFI DA AFUWARSA GARESU DA ABINDA YA UMARCE SU DASHI)

88. Yayin da suka shiga gareshi sai Sukace, "Ya wannan ma'aji, yunwa ta shafe mu mu da jama'armu, mun zoda tarkace kwaimawa, (wato mummuna, wato dirhamai ne" yan jabu,) to, sai ka cika mana mudu, kayi sadaka garemu, (wato ka kau da kanka a bisa munin kuɗinmu,) haƙiƙa Ubangiji yana sakawa masu sadaka".

89. (To sai yaji tausayinsu ya yaye shamakin da yake tsakaninsa dasu, sannan yace dasu don kurustawa,) "Shin kun san abinda kuka aikata ga Yusufa (na duka da sayarwa da wanin wancananka) da ɗan'uwansa (na daga zaluntar da kukayi masa bayan ya rabu da ɗan'uwansa,) yayin da baku san irin yadda Annabi Yusufu zai zama ba?".

90. Sai Sukace, (bayan sun shedashi, yayin daya bayyana musu daga tadodinsa,) "Haƙiƙa lalle kaine Annabi Yusufu, yace, nine Yusufu, wannan ɗan uwana ne Allah yayi ni'ima garemu (ya tara mu) haƙiƙa lamarin wanda yaji tsoron Allah (ya haƙura bisa abinda ya same shi) haƙiƙa Ubangiji baya tozarta ladan masu aiki".

91. Sukace, "Wo-ho-ho! Wallahi lalle Allah yafifita ka a kanmu (da mulki da waninsa, haƙiƙa mun kasance lalle masu kuskure ne a cikin al'amarinka (saboda haka ya rusunar da mu gabanka".)

92. Yace, "Bazargi a gareku a yau, Allah yayi muku gafara, shine mafi jinkan masu jinƙai".(HALACCIN HIRƘA WATO YANKIN SUFAYE WANDA SUKE BAIWA MURIDI DON NEMAN ALBARKA DASHIGARWA DASHI CIKIN ZIKIRIN TAFARKINSU)

93. (Ya tambaye su ga mahaifinsa, Sukace, "Idanuwansa sun duhunce") Yace, "ku tafi da rigata wannan, (Itace rigar Annabi Ibrahim Alaihissalam wacce ya daurata zamanin da aka shigar dashi wuta, ta kasance tana cikin wuyansa a kururrumar rijiya, an yi masa laya da ita [1] (ita daga aljanna take da aka umarci Jibrilu Alaihissalam ya daura wa Annabi Ibrahim Alaihissalam saboda akwai ƙanshin aljanna a cikinta, baza ajefa shi a bisa abin jarraba ba face Allah ya bashi lafiya,) [2] "Ku jefa ta a bisa fuskar mahaifina ya zama mai gani"[3]. (ANNABI YAKUBU ALAIHISSALAM ALHALI MAI ALBISHIR YAZO MASA-AKWAI SHI A CIKIN MITUJIZAR JIN SHEKAR KANSHI DAGA WURI MAI NISA KAMAR WAƊANDA SHEHU IBNIL ARABI YAKE KIRANSU AKADABUL-SHAMMI, MASU SHEKAR KANSHI)

94. Yayin dayan karafka (wato 'yan kwarami suka fito daga Arishi;[4]. Misra zasu koma gida wato garuruwan Kan'ana wato shine Nabulusa a yanzu.) Sai ubansu yace (ga waɗanda suke kusa dashi na daga "ya" yansa da jikoki,) "Ni ina jin ƙanshin Annabi Yusufa (Alaihissalam) ba don zaku dangana ni izuwa wauta ba". (Ubangiji ya sadashi da Wannan ƙanshin da izininsa daga tafiyar kwana uku ko takwas.)

95. Sai Sukace, (dashi,) "Wallahi haƙiƙa kai dai kana cikin kuskuranka daɗaɗɗe" (na faifayewarka a cikin sonsa, da kaunar saduwa dashi tareda nisan lokaci".)

1) A cikin wannan akwai hataccin rataya layu awuya da syka kunshi ayako wata hikima ko wani abu mai girma gurin Allah. - Sanajiy -2) Hakana shi yankin dasufaye suke baiwa muri-dansu tana kunshe da asirin wilaya da yake ciki, wanda s'ika bashi wannan yanki zai gamu da tasiri na yanzu-yanzu, idan ta zama yanki ce ta tahakika, yankin tabarruki da ta-shabbuhi. bazasu wofintada tabarruki na daga wannan albarka ba, kamar yadda shehu Jabir yake fadar haka a cikin littafinsa: Usulul-Awliyai - Sanajiy -3) tunda wannan riga ta Annabi Yusufu tayi tasiri a idanun mahaifinsa, to, ba ma'ana ga musun hirƙar sufaye, wacce suke daurawa muridai, saitaurin kai kadai da kin waliyyai, Allah ya kiyashemu. 4) Gari ne sanan ne akarshen garuruwan misra, farkon garuruwan sham

فَلَمَّآ أَن جَآءَ ٱلْبَشِيرُ أَلْقَىٰهُ عَلَىٰ وَجْهِهِۦ فَٱرْتَدَّ بَصِيرًا ۖ قَالَ أَلَمْ
أَقُل لَّكُمْ إِنِّىٓ أَعْلَمُ مِنَ ٱللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿96﴾ قَالُوا۟ يَٰٓأَبَانَا
ٱسْتَغْفِرْ لَنَا ذُنُوبَنَآ إِنَّا كُنَّا خَٰطِـِٔينَ ﴿97﴾ قَالَ سَوْفَ
أَسْتَغْفِرُ لَكُمْ رَبِّىٓ ۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿98﴾ فَلَمَّا دَخَلُوا۟ عَلَىٰ
يُوسُفَ ءَاوَىٰٓ إِلَيْهِ أَبَوَيْهِ وَقَالَ ٱدْخُلُوا۟ مِصْرَ إِن شَآءَ ٱللَّهُ
ءَامِنِينَ ﴿99﴾ وَرَفَعَ أَبَوَيْهِ عَلَى ٱلْعَرْشِ وَخَرُّوا۟ لَهُۥ سُجَّدًا ۖ
وَقَالَ يَٰٓأَبَتِ هَٰذَا تَأْوِيلُ رُءْيَٰىَ مِن قَبْلُ قَدْ جَعَلَهَا
رَبِّى حَقًّا ۖ وَقَدْ أَحْسَنَ بِىٓ إِذْ أَخْرَجَنِى مِنَ ٱلسِّجْنِ وَجَآءَ بِكُم
مِّنَ ٱلْبَدْوِ مِنۢ بَعْدِ أَن نَّزَغَ ٱلشَّيْطَٰنُ بَيْنِى وَبَيْنَ إِخْوَتِىٓ ۚ
إِنَّ رَبِّى لَطِيفٌ لِّمَا يَشَآءُ ۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْعَلِيمُ ٱلْحَكِيمُ ﴿100﴾
۞ رَبِّ قَدْ ءَاتَيْتَنِى مِنَ ٱلْمُلْكِ وَعَلَّمْتَنِى مِن تَأْوِيلِ ٱلْأَحَادِيثِ ۚ
فَاطِرَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ أَنتَ وَلِىِّۦ فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ ۖ
تَوَفَّنِى مُسْلِمًا وَأَلْحِقْنِى بِٱلصَّٰلِحِينَ ﴿101﴾ ذَٰلِكَ مِنْ أَنۢبَآءِ
ٱلْغَيْبِ نُوحِيهِ إِلَيْكَ ۖ وَمَا كُنتَ لَدَيْهِمْ إِذْ أَجْمَعُوٓا۟ أَمْرَهُمْ وَهُمْ
يَمْكُرُونَ ﴿102﴾ وَمَآ أَكْثَرُ ٱلنَّاسِ وَلَوْ حَرَصْتَ بِمُؤْمِنِينَ ﴿103﴾

رُبع

96. Yayin da mai albishir yazoda riga (shine Yahuda, da can shine ya dauki rigar jini, sai yaso ya faranta masa tamfar daya bakanta masa,) saiya jefa rigar nan a bisa fuskarsa, to, sai yakomo mai gani tangaran, sai yace, "BAnce da ku, haƙiƙa ni na san abinda baku sani badaga Allah?.

97. Sukace "Ya babanmu, nema mana gafarar zunubanmu wurin Ubangiji, haƙiƙa mu, mun kasance masu kuskure".

98. Sai yace, "Da sannu zan nema muku gafarar Ubangijina, haƙiƙa shi, shine mai gafara mai jinƙai" (yajinkirta wannan izuwa sahur donya kasance mafi kusa daga amsawa, sannan suka fuskanta izuwa Misra, Annabi Yusufu ALaihissalam da manyan gari suka fito saboda taryensu.)

(FASSARAR MAFARKIN ANNABI YUSUFU ALAIHISSALAM TA TUN FARKO)

99. Yayin da suka shiga a bisa Annabi Yusufu (Alaihissalam a cikin haima tasa,) saiya tattara mahaifinsa da mahaifiyarsa izuwa gareshi, yace, "Ku shigo Misra in Allah ya yarda amin-tattu (suka shigo ya zauna a kan karagar mulkinsa)

100. Ya ɗaukaka iyayensa a kan gadon mulki suka faɗi suna masu gaisuwa a gareshi (ta sunkuyar da wuya iTace gaisuwar a wancananka lokaci,) yace ya babana, wannan shine fassarar ma-farkina tun dauri, Allah yasanya ta gaskiya, ya kyautata min dayafitar dani daga kurkuku, (bai ce daga kururrumar rijiyaba don kada ya kunyatar da "yan uwansa, saboda kurkukun bana "yan uwansa ba ne) ya kawo ku daga ƙauye bayan shaiɗan yayi ɓarna tsakanina da "yan uwana, haƙiƙa Ubangijina ma» taushine ga abinda yake so, haƙiƙa shine masani (da halitta) gwani (cikin aiki. Ubansa ya zauna wurinsa shekara ashirin da hudu, muddar rabuwarsu kuma shekara goma sha takwas, ajali yazo masa yayi wa Annabi Yusufu Alaihissalam wasiyyaya ɗauke shi yabinne shi can tareda ubansa, ya dace ɗan uwan ta gwai takarsa "ISU" ya rasu saiya binnesu akabari ɗaya. ya ɗauke shi da kansa ya je ya binne shi a (Halil) can a Baitul - Maƙadisi, sannan yakomo izuwa Misra, ya zauna shekara ashirin da uku bayansa, yayin da al'amarinsa ya cika, sai yayi bege izuwa mulki madauwami.)

(KARSHEN LAMARIN ANNABI YUSUFU ALAIHISSALAM)

101. Yaċe, "Ubangiji haƙiƙa ka bani daga mulki, ku sanar dani daga fassarar mafarkai, Ya mahaliccin sammai da ƙassai, Kaine majiɓincina a duniya da lahira, ka ƙarbi raina ina Musulmi. ka riskar dani da mutanen kirki (salihai na iyayena, ya rayu kwana bakwai bayan wannan, ya rasu yana dan shekara ɗari da ashirin. Mutanen Masar sukayi rowa a cikin ƙabarinsa, suka sa shi a cikin sundukin marmara, suka binne shi a samancin Nil, don albarka tasa ta gama gyaffensa. Tsarki ya tabbata ga wanda mulkinsa baya karewa.)

ABINDA ƘISSA TAKE NUNI GARESHI TO SHINE TA KARIMIN MANZON ALLAH DASHI DA KIRARI GA ALƘUR,ANI

102. Wancananka abin ambato (na daga ƙissar annabi Yusufu Alaihissalam) yana daga labaran gaibu, muke aiko shi gareka, (Sallallahu alaika wasallama,) baka kasance gurinsu ba (su "yan uwan Annabi Yusufu Alaihissalam,) yayin da suka kulla gezata lamarinsu a cikin kaidi ga Annabi Yusufu (Alaihissalam) alhali suna makirci (dashi, mune muka sanar dakai ta fuskar wahayi.)

103. Yawaicin mutane basu kasance muminai ba koda kayi kwaɗayi cikin imaninsu.

وَمَا تَسْـَٔلُهُمْ عَلَيْهِ مِنْ اَجْرٍ اِنْ هُوَ إِلَّا ذِكْرٌ لِّلْعَٰلَمِينَ ﴿104﴾
وَكَأَيِّن مِّنْ ءَايَةٍ فِي السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ يَمُرُّونَ عَلَيْهَا
وَهُمْ عَنْهَا مُعْرِضُونَ ﴿105﴾ وَمَا يُؤْمِنُ أَكْثَرُهُم بِاللَّهِ
إِلَّا وَهُم مُّشْرِكُونَ ﴿106﴾ أَفَأَمِنُوا أَن تَأْتِيَهُمْ غَاشِيَةٌ مِّنْ عَذَابِ اللَّهِ
أَوْ تَأْتِيَهُمُ السَّاعَةُ بَغْتَةً وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿107﴾ قُلْ هَٰذِهِ سَبِيلِي
أَدْعُوا إِلَى اللَّهِ عَلَىٰ بَصِيرَةٍ أَنَا وَمَنِ اتَّبَعَنِي وَسُبْحَٰنَ اللَّهِ
وَمَا أَنَا مِنَ الْمُشْرِكِينَ ﴿108﴾ وَمَا أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ إِلَّا رِجَالًا
يُوحَىٰ إِلَيْهِم مِّنْ أَهْلِ الْقُرَىٰ أَفَلَمْ يَسِيرُوا فِي الْأَرْضِ
فَيَنظُرُوا كَيْفَ كَانَ عَاقِبَةُ الَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ وَلَدَارُ
ءَالْاخِرَةِ خَيْرٌ لِّلَّذِينَ اتَّقَوْا أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿109﴾ * حَتَّىٰ
إِذَا اسْتَيْـَٔسَ الرُّسُلُ وَظَنُّوا أَنَّهُمْ قَدْ كُذِّبُوا جَاءَهُمْ نَصْرُنَا
فَنُنجِي مَن نَّشَاءُ وَلَا يُرَدُّ بَأْسُنَا عَنِ الْقَوْمِ الْمُجْرِمِينَ ﴿110﴾
لَقَدْ كَانَ فِي قَصَصِهِمْ عِبْرَةٌ لِّأُوْلِي الْأَلْبَٰبِ مَا كَانَ حَدِيثًا
يُفْتَرَىٰ وَلَٰكِن تَصْدِيقَ الَّذِي بَيْنَ يَدَيْهِ وَتَفْصِيلَ
كُلِّ شَيْءٍ وَهُدًى وَرَحْمَةً لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿111﴾

ثمن

104. Baka tambayarsu lada bisa ida alƙur'ani, shi alƙur'ani bai kasance ba, illa gargaɗi ga talikai.
105. Da yawa daga aya (mai nuna girman Allah cikin sammai da ƙassai, suna shudewa a kanta suna ganinta alhali su masu bijirewa ne ga buranta.
106. Yawaicinsu basa bada gaskiya da Allah (da cewa shine mahalicci mai azurta wa) face suna masu shirka dashi (da bautar gumaka, waɗanda suke faɗa a cikin talbiyyarsu, Labbaika-lasharika-laka illa shankan-huwa- laka.)
107. To, shin sun amince ne yanki na azabar Allah ya sauka a garesu, ko kuma alƙiyama tazo musu baraɓe alhali su basu san lokacin zuwanta ba!
108. Cene (dasu) "Wannan iTace hanyata, ina kira izuwa,addinin Allah a bisa hujja (mabayyaniya,) ni da wanda yabi ni. Tsarki ya tabbata ga Ubangiji (ga buran shariki,) ni ban kasance daga masu shirka ba".

(SASHIN MANUFOFIN WANNAN KISSA)

109. Bamu aiko gabanka ba face mazaje da ake aiko su izuwa garesu ba Mala'iku badaga mutanen birni, (domin su sun fi ilimi sun fi hankali, sabanin mutanen ƙauye saboda wautarsu da karancin hankalinsu,) shin basuyi tafiyabane cikin ƙasa su dubasu ga kaka ƙarshen waɗanda suke gabansu ta kasance, lalle gidan lahira (Aljanna,) shine mafi amfani ga waɗanda sukaji tsoron Allah, shin ba kwayi hankali (ku bada gaskiya ba) (Taimakon manzannin nan yayi jinkiri)
110. Har zamanin da manzannin nan suka ɗebe haso suka tabbatacewa an ƙaryata su, (wato mabiya Annabawan nan suka zaci saba alƙawarin da Annabawa sukayi musu,) to, saitaimakonmu yazo musu, sai muka tserar da wanda muka ga dama, ba a mayar da azabarmu ga buran mutane mushirikai.
111. Lalle akwai izna a cikin labartawar nan ta manzanni ga ma'abuta hankula, wannan alƙur'ani bai kasance zance da ake ƙirƙirar sa ba, shi dai ya kasance gasgatawar abinda yake gabansa (na littattafai,) da rar- rabe kowane abu da ake bukata izuwa gareshi na addini, dashiriya da jinkai ga mutane muminai.

13 سُورَةُ الرَّعْدِ مَدَنِيَّةٌ
وَهِيَ أَرْبَعٌ وَأَرْبَعُونَ آيَةً 44

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

الٓمٓر تِلْكَ ءَايَٰتُ الْكِتَٰبِ وَالَّذِيٓ أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ الْحَقُّ
وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ النَّاسِ لَا يُؤْمِنُونَ ۝1 اللَّهُ الَّذِي رَفَعَ السَّمَٰوَٰتِ
بِغَيْرِ عَمَدٍ تَرَوْنَهَا ثُمَّ اسْتَوَىٰ عَلَى الْعَرْشِ وَسَخَّرَ الشَّمْسَ وَالْقَمَرَ
كُلٌّ يَجْرِي لِأَجَلٍ مُّسَمًّى يُدَبِّرُ الْأَمْرَ يُفَصِّلُ الْآيَٰتِ لَعَلَّكُم بِلِقَآءِ رَبِّكُمْ
تُوقِنُونَ ۝2 وَهُوَ الَّذِي مَدَّ الْأَرْضَ وَجَعَلَ فِيهَا رَوَٰسِيَ وَأَنْهَٰرًا وَمِن
كُلِّ الثَّمَرَٰتِ جَعَلَ فِيهَا زَوْجَيْنِ اثْنَيْنِ يُغْشِي الَّيْلَ النَّهَارَ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ
لَآيَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَتَفَكَّرُونَ ۝3 وَفِي الْأَرْضِ قِطَعٌ مُّتَجَٰوِرَٰتٌ وَجَنَّٰتٌ
مِّنْ أَعْنَٰبٍ وَزَرْعٌ وَنَخِيلٌ صِنْوَانٌ وَغَيْرُ صِنْوَانٍ تُسْقَىٰ بِمَآءٍ وَٰحِدٍ
وَنُفَضِّلُ بَعْضَهَا عَلَىٰ بَعْضٍ فِي الْأُكُلِ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَآيَٰتٍ
لِّقَوْمٍ يَعْقِلُونَ ۝4 ۞ وَإِن تَعْجَبْ فَعَجَبٌ قَوْلُهُمْ أَءِذَا كُنَّا تُرَٰبًا
أَءِنَّا لَفِي خَلْقٍ جَدِيدٍ ۝5 أُوْلَٰٓئِكَ الَّذِينَ كَفَرُواْ بِرَبِّهِمْ وَأُوْلَٰٓئِكَ
الْأَغْلَٰلُ فِيٓ أَعْنَاقِهِمْ وَأُوْلَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ النَّارِ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ۝6

رُبْع

Suratul Ra'adi

A Madina Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Arba'in Da Hudu (44)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabadaya, mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

(ALƘUR'ANI GASKIYA NE, ALLAH MAI IKONEBISA KOMAI)

'Wannan sura ta kunshi tauhidi da mikuwar kira zuwa tauhidi da yawa yawa daga kirarin Allah da rarrashi ga ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wasallama'

1. A.L.M.R. Allah ne masani da abinda yake nufi da wannan kalma, waɗannan ayoyi, ayoyi ne na daga littafi (alƙur'ani) abinda aka saukar izuwa gareka daga Ubangijinka (na alƙur'ani) shine gaskiya wanda ba kokwanto a kansa, sai dai yawaicin mutane basu bada gaskiya (cewa shi daga Allah yake) ba.

(MANA KAN ƘUDURAR OBANGIJI DA RADDI, GA"YAN DABI'A)

2. Allah ne wanda ya daga sammai bada ginshikai da kuke ganin ta ba, sannan yayi daidai kan Al'arshi, (daidaito daya dace dashi,) ya horc rana da wata kowanne daga cikinsu yana gudana a cikin falakinsa izuwa lokaci abin ambato (shine ranar alƙiyama,) Allah yana shirya al'amari na sama da kasa, (da rayuwa da matarwa da bayarwa da wulakantarwa da wanin wannan na daga nau'o'i, juye-juyen Allah don ku sakankance da saduwa da Ubangiji (da tashin alƙiyama.)
3. shine wanda ya shinfiɗe ƙassai,ya halicci duwarwatsu tabbatattu a cikintada ƙoramu daga dukkan "ya'yan itaciya, yasanya nau'i bibiyu (misalin zaƙi da ɗaci, da kaushi da laushi, yana lulluɓe dare da rana. Haƙiƙa a cikin wancananka akwai ayoyi (masu nuna ikon Allah) ga mutane masu tunani (a cikin aikin Allah.)
4. A' cikin ƙasa akwai gurare dabandaban masu ma ƙotaka da juna, akwai kyakkyawar ƙasa da mummuna (duka wannan yana daga dalilan ikon Allah,) da gonakai na inabai da hatsi da dabinai "yan tagwaye da wanin "yan tagwaye da ake shayar da itada ruwa guda ɗaya, muna fifita ba'alinta a bisa ba'ali a cikin ɗanɗani. A cikin wancananka akwai ayoyi ga mutane masu hankali.

(SASHIN MAGANGANUNSU DA SAKAMAKO A KANTA)

5. Idan kayi mana ki, to, abin mana ki ne faɗin masu musun tashi, yanzu idan mun kasance turɓaya, yanzu haƙiƙa mu, muna cikin halitta sabuwa?
6. Waɗancananka sune waɗanda suka kafirtada Ubangijinsu wadancananka ne ƙuƙumai suke cikin wuyayinsu, waɗancananka ne"yan wuta, su madauwama ne a cikinta.

وَيَسْتَعْجِلُونَكَ بِٱلسَّيِّئَةِ قَبْلَ ٱلْحَسَنَةِ وَقَدْ خَلَتْ مِن قَبْلِهِمُ
ٱلْمَثُلَٰتُ وَإِنَّ رَبَّكَ لَذُو مَغْفِرَةٍ لِّلنَّاسِ عَلَىٰ ظُلْمِهِمْ
وَإِنَّ رَبَّكَ لَشَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ﴿7﴾ وَيَقُولُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ
لَوْلَآ أُنزِلَ عَلَيْهِ ءَايَةٌ مِّن رَّبِّهِۦٓ إِنَّمَآ أَنتَ مُنذِرٌ وَلِكُلِّ
قَوْمٍ هَادٍ ﴿8﴾ ٱللَّهُ يَعْلَمُ مَا تَحْمِلُ كُلُّ أُنثَىٰ وَمَا تَغِيضُ
ٱلْأَرْحَامُ وَمَا تَزْدَادُ وَكُلُّ شَيْءٍ عِندَهُۥ بِمِقْدَارٍ ﴿9﴾
عَٰلِمُ ٱلْغَيْبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ ٱلْكَبِيرُ ٱلْمُتَعَالِ ﴿10﴾ سَوَآءٌ مِّنكُم مَّنْ
أَسَرَّ ٱلْقَوْلَ وَمَن جَهَرَ بِهِۦ وَمَنْ هُوَ مُسْتَخْفٍ بِٱلَّيْلِ
وَسَارِبٌ بِٱلنَّهَارِ ﴿11﴾ لَهُۥ مُعَقِّبَٰتٌ مِّنۢ بَيْنِ يَدَيْهِ وَمِنْ خَلْفِهِۦ
يَحْفَظُونَهُۥ مِنْ أَمْرِ ٱللَّهِ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُغَيِّرُ مَا بِقَوْمٍ حَتَّىٰ يُغَيِّرُواْ
مَا بِأَنفُسِهِمْ وَإِذَآ أَرَادَ ٱللَّهُ بِقَوْمٍ سُوٓءًا فَلَا مَرَدَّ لَهُۥ وَمَا لَهُم
مِّن دُونِهِۦ مِن وَالٍ ﴿12﴾ هُوَ ٱلَّذِي يُرِيكُمُ ٱلْبَرْقَ خَوْفًا
وَطَمَعًا وَيُنشِئُ ٱلسَّحَابَ ٱلثِّقَالَ ﴿13﴾ وَيُسَبِّحُ ٱلرَّعْدُ بِحَمْدِهِۦ
وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ مِنْ خِيفَتِهِۦ وَيُرْسِلُ ٱلصَّوَٰعِقَ فَيُصِيبُ بِهَا
مَن يَشَآءُ وَهُمْ يُجَٰدِلُونَ فِي ٱللَّهِ وَهُوَ شَدِيدُ ٱلْمِحَالِ ﴿14﴾

(WANNAN AYA TA SAUKA A CIKIN GAGGAWAR SAUKAR AZABADA IZGILI)

7. Suna gaggauto dakai da azabar gaban rahama, alhali uƙubobi ta wuce daga gabansu haƙiƙa Ubangijinka lalle mai gafara ne bisa mutane tareda zaluncinsu, haƙiƙa Ubangijinka mai tsananin uƙubane (ga waɗanda suka saɓe shi.)

(MATSAYIN MAKIRAYA IZUWA ALLAH DA KIRARI GA ALLAH)

8. Waɗanda suka kafirta suna cewa, "Donme ba a saukar da aya gareshi ba; Annabi (Sallallahu alaihi wasallama kamar sanda da hannu da taguwa?" Ubangiji yace, "Kai mai gargaɗi ne kawai, (zuwa da ayoyi ba lalle ne a kan ka ba,) kowane jama'a suna da mai shiryar dasu".

WANI ABU NA DAGA MABAYYANAR ILIMIN UBANGIJI DA HIKIMARSA)

9. Allah ne yasan abinda kowacc mace take dauke dashi (namiji ko mace, dayako biyu da wanin wannan,) da abinda mahaifa ta tauye (na daga muddar ciki,) da abinda take ƙarawa (daga gareshi) kowane abu gurin Allah yana da iyaka.
10. Masanin asirin fake dana sarari, Maigirma Maɗaukaki.
11. wanda ya ɓoye magana ko ya bayyana daga cikinku daidai ne (a cikin sanin Allah) da wanda yake mai buya da dare da wanda yake tafiya a fili da rana.

(RAƘIBU DA ATIDU DA IRE-IRENSU DAGA MALAIKU)

12. Mala'iku masu gadi sun tabbata ga mutum, (wato sune Raƙibu da Atidu da ake faɗa) daga gabansa da bayansa suna kiyaye shi daga al'amarin Allah, (wato aljannu ko waninsu) haƙiƙa Ubangiji ba yajirkita ni'imar da take ga mutane sai sun jirkita abinda yake kawukansu (na daga hali Mai - kyau da saɓo,) idan Ubangiji yanufi azabada mutane ba juyarwa ga azabar nan (daga masu gadin nan) basu da wani majibinci ba Allab ba (dazai hana musu azabar Allah.)

(WANI ABU DAGA MABAYYANAR IKON ALLAH DA ALLANTAKARSA)

13. shine wanda yake nuna muku walƙiya don tsoron tsawa ga matafiya da ƙaunar ruwa ga mazauna, yake farar da gizagizai masu nauyi da ruwa .
14. Tsawa tana yin tasbihi da godiyar Ubangiji, Mala'iku sunayi saboda tsoron Allah, yana aiko tsawawwaki, wutada take fita daga girgije ya sami wanda yaga dama da ita (ta ƙone shi, ta sauka a kan wani mutum da Annabi ya tura wani mutum ya kirawo shi, sai yace waye Rasulullahi, yace kuma waye Allah, na zinare ne ko azurfa ko tagulla.? sai tsawa ta sauko a kansa saita tafi da ƙoƙon kansa) alhali su kafirai suna jayayya da Manzon Allah a cikin Allah, to Allah kuwa mai tsananin ƙarfi ne.

لَهُۥ دَعْوَةُ الْحَقِّ وَالَّذِينَ يَدْعُونَ مِن دُونِهِۦ لَا يَسْتَجِيبُونَ لَهُم بِشَيْءٍ
إِلَّا كَبَاسِطِ كَفَّيْهِ إِلَى الْمَآءِ لِيَبْلُغَ فَاهُ وَمَا هُوَ بِبَالِغِهِۦ وَمَا دُعَآءُ
الْكَافِرِينَ إِلَّا فِي ضَلَالٍ ﴿15﴾ وَلِلَّهِ يَسْجُدُ مَن فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ
طَوْعًا وَكَرْهًا وَظِلَالُهُم بِالْغُدُوِّ وَالْآصَالِ ﴿16﴾ * قُلْ مَن رَّبُّ
السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ قُلِ اللَّهُ قُلْ أَفَاتَّخَذتُّم مِّن دُونِهِۦ أَوْلِيَآءَ
لَا يَمْلِكُونَ لِأَنفُسِهِمْ نَفْعًا وَلَا ضَرًّا قُلْ هَلْ يَسْتَوِي الْأَعْمَىٰ
وَالْبَصِيرُ أَمْ هَلْ تَسْتَوِي الظُّلُمَاتُ وَالنُّورُ ﴿17﴾ أَمْ جَعَلُوا لِلَّهِ شُرَكَآءَ
خَلَقُوا كَخَلْقِهِۦ فَتَشَابَهَ الْخَلْقُ عَلَيْهِمْ قُلِ اللَّهُ خَالِقُ
كُلِّ شَيْءٍ وَهُوَ الْوَاحِدُ الْقَهَّارُ ﴿18﴾ أَنزَلَ مِنَ السَّمَآءِ مَآءً
فَسَالَتْ أَوْدِيَةٌۢ بِقَدَرِهَا فَاحْتَمَلَ السَّيْلُ زَبَدًا رَّابِيًا وَمِمَّا تُوقِدُونَ
عَلَيْهِ فِي النَّارِ ابْتِغَآءَ حِلْيَةٍ أَوْ مَتَاعٍ زَبَدٌ مِّثْلُهُۥ كَذَٰلِكَ يَضْرِبُ اللَّهُ
الْحَقَّ وَالْبَاطِلَ فَأَمَّا الزَّبَدُ فَيَذْهَبُ جُفَآءً وَأَمَّا مَا يَنفَعُ النَّاسَ
فَيَمْكُثُ فِي الْأَرْضِ كَذَٰلِكَ يَضْرِبُ اللَّهُ الْأَمْثَالَ ﴿19﴾ لِلَّذِينَ اسْتَجَابُوا
لِرَبِّهِمُ الْحُسْنَىٰ وَالَّذِينَ لَمْ يَسْتَجِيبُوا لَهُۥ لَوْ أَنَّ لَهُم مَّا فِي الْأَرْضِ جَمِيعًا وَمِثْلَهُۥ
مَعَهُۥ لَافْتَدَوْا بِهِۦ أُولَٰٓئِكَ لَهُمْ سُوٓءُ الْحِسَابِ وَمَأْوَاهُمْ جَهَنَّمُ وَبِئْسَ الْمِهَادُ ﴿20﴾

سجدة
ثمن

15. Kiran gaskiya yana ga Allah (wato kalmar La'ilaha illallahu,) waɗanda suke bautawa wanin Allah, bazasu amsa musu da wani abu ba cikin abinda suke nema, sai irin amsawar mai shinfiɗa tafukansa izuwa ruwa a kan gaɓar rijiya, yana kiransa, dan ruwan ya isa bakinsa, daga rijiya, shi bazai isa izuwa bakinsa ba har abada, addu'ar kafirai bata kasance ba sai a cikin halaka.
16. Duk abinda yake cikin sammai da ƙassai yana sajada ga Allah (ko yaso ko ya ƙi, inuwoyinsu (suna sajada ga Allah) safiya dayammaci.

Sajada

17. Cene (dasu) "Waye Ubangijin sammai da ƙassai?" Cene "Allah ne, in sun yi shuru,) cene (dasu) donme kuka riƙi gumaka ba Allah ba, waɗanda basu mallaki cuta ko amfani ga kansu ba? Cene, "Shin makaho da mai gani sayi daidai, (wato. mumin da kafiri,) ko kuwa duffan kafirci za suyi daidai da imani", (baza suyi daidai ba.)
18. Ko sun sanya sharikaine ga Allah dasuke halitta kamar irin halittar Allah, sai halitta ya Rikita garesu, Cene (dasu) "Allah ne mahaliccin komai, shine mawadaci mai rinjaye.

KWATANCIN GASKIYA DA MA'ABOTANTA DAƘARYA DA MA'ABOTANTA)

19. Ubangiji ya saukar da ruwa daga sama sai zazaiku suka kwarara da gwargwadon faɗinta, sai ruwa ya ɗauki kunfa mai banbaro a kansa, akwai daga abinda kuke hura wuta a kansa (na daga jauharorin ƙasa kamar zinare da azurfa,) don neman ado ko abin amfani, akwai kunfa kamarsa (wanda zigazigi yakore shi,) to, hakana Allah yake sanya misalin ƙarya da gaskiya, amma kunfar ruwa (da abinda hura wuta a kansa na daga jauharori) zai tafi a banza, amma abindazai amfani mutane (na daga ruwa da jauharori,) to, zai zauna a cikin ƙasa (zamani mai tsawo, hakana ƙarya take watsewa gaskiYakuma take tabbata abadan sarmadan,) hakana Allah yake bayyanawa mutane misalce -misalce.
20. Aljanna ta tabbata ga waɗanda suka amsawa Ubangijinsu (da ɗa"a,) waɗanda basu amsa bakuwa, da abinda yake cikin ƙasa bakiɗaya nasune da misalinsa taredashi, dasun yi fansa dashi daga azaba, Wancananka mummunan sakamako yana garesu, jahannama ce makomarsu, tur da ita shinfiɗa!

حزب

* أَفَمَن يَعْلَمُ أَنَّمَا أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ الْحَقُّ كَمَنْ هُوَ أَعْمَىٰٓ إِنَّمَا يَتَذَكَّرُ
أُوْلُواْ الْأَلْبَٰبِ ﴿21﴾ الَّذِينَ يُوفُونَ بِعَهْدِ اللَّهِ وَلَا يَنقُضُونَ الْمِيثَٰقَ ﴿22﴾
وَالَّذِينَ يَصِلُونَ مَا أَمَرَ اللَّهُ بِهِۦ أَن يُوصَلَ وَيَخْشَوْنَ رَبَّهُمْ وَيَخَافُونَ
سُوٓءَ الْحِسَابِ ﴿23﴾ وَالَّذِينَ صَبَرُواْ ابْتِغَآءَ وَجْهِ رَبِّهِمْ وَأَقَامُواْ الصَّلَوٰةَ
وَأَنفَقُواْ مِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ سِرّاً وَعَلَانِيَةً وَيَدْرَءُونَ بِالْحَسَنَةِ السَّيِّئَةَ
أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمْ عُقْبَى الدَّارِ ﴿24﴾ جَنَّٰتُ عَدْنٍ يَدْخُلُونَهَا وَمَن صَلَحَ
مِنْ ءَابَآئِهِمْ وَأَزْوَٰجِهِمْ وَذُرِّيَّٰتِهِمْ وَالْمَلَٰٓئِكَةُ يَدْخُلُونَ
عَلَيْهِم مِّن كُلِّ بَابٍ سَلَٰمٌ عَلَيْكُم بِمَا صَبَرْتُمْ فَنِعْمَ عُقْبَى الدَّارِ ﴿25﴾
وَالَّذِينَ يَنقُضُونَ عَهْدَ اللَّهِ مِنۢ بَعْدِ مِيثَٰقِهِۦ وَيَقْطَعُونَ مَا أَمَرَ
اللَّهُ بِهِۦ أَن يُوصَلَ وَيُفْسِدُونَ فِي الْأَرْضِ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ اللَّعْنَةُ
وَلَهُمْ سُوٓءُ الدَّارِ ﴿26﴾ اللَّهُ يَبْسُطُ الرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقْدِرُ
وَفَرِحُواْ بِالْحَيَوٰةِ الدُّنْيَا وَمَا الْحَيَوٰةُ الدُّنْيَا فِي الْآخِرَةِ إِلَّا
مَتَٰعٌ ﴿27﴾ وَيَقُولُ الَّذِينَ كَفَرُواْ لَوْلَآ أُنزِلَ عَلَيْهِ ءَايَةٌ مِّن رَّبِّهِۦ
قُلْ إِنَّ اللَّهَ يُضِلُّ مَن يَشَآءُ وَيَهْدِيٓ إِلَيْهِ مَنْ أَنَابَ ﴿28﴾ الَّذِينَ ءَامَنُواْ
وَتَطْمَئِنُّ قُلُوبُهُم بِذِكْرِ اللَّهِ أَلَا بِذِكْرِ اللَّهِ تَطْمَئِنُّ الْقُلُوبُ ﴿29﴾

21. Yanzu wanda yasan haƙiƙa abinda aka saukar izuwa gareka daga Ubangijinka gaskiya ne (ya bada gaskiya dashi) kamar wanda yake shi makaho ne (bai san haka ba ba re ya bada gaskiya dashi, a'a!) Haƙiƙa ma'abuta hankula sune suke wa'azantuwa.

SU WAYE ULUL-ALBABI, MEYE SAKAMAKONSU, DA FALALAR CIKA ALKAWARI?)

22. Sune waɗanda suke cikawa da alƙawarin Allah (wanda aka karɓa garesu a Alamirzarri, da kuma dukkan alƙawari,) basa warware alƙawari (da barin imani ko farillai.)

(FALALAR SADAR DA ZUMUNTA)

23. Sune waɗanda suke sada abinda Ubangiji yayi nufin sadashi, (na daga imani mai cikakken shamda da mkunai da ladabai, suke sada zumuntada waninta,) suna tsoron Ubangijinsu, suna tsoron mummunan sakamako.

(TSARKAKE AIKI SABODA ALLAH)

24. Da waɗanda suka daure (a kan ɗa'a da bala'i da saɓo,) don neman yardar Ubangijinsu, (ba don wani abu na daga bukkace- bukacen duniya ba,) suka tsayar da salla, suka ciyar daga abinda muka azurta musu asiri da bayyane, suna ijewar mummunan aiki da aiki nagari, (wato wautada hankali, cutada haƙuri,) waɗancananka kyakkyawan ƙarshe ya tabbata garesu (a lahira.)

(FALALAR DANGANTUWA IZUWA AHLUL-LAHI-WALIYYAI)

25. Aljannar zama zasu shige ta su da wanda ya bada gaskiya daga iyayensu, da matayensu,da zuriyyoyinsu (koda basuyi aiki da aikinsu ba, zasu kasance cikin darajojinsu don girmama wa a garesu,) Mala'iku zasu dinga shiga a garesu ta kowace ƙofa, (daga ƙofofin aljanna, saboda barka da arziki, zasu dinga cewa,) Salamu alaikum, wannan sakamako saboda dauriyarkune (a duniya,) madalla ƙarshen gida aljanna.

(SHU'UMIN WARWARE ALƘAWARI KAMAR FITA DAG DARIKA)

26. Waɗanda suke warware alƙawarin Allah bayan ƙudura shi suke yanke abinda Allah yayi umarni a sadar dashi, suke barna a bayan ƙasa (da kafirici da sabo,) waƙancananka, la'ana ta tabbata garesu mummunar makoma na garesu jahannama.

(WANI ABU DAGA SIFOFINSU HAR YAU)

27. Allah yana yalwatawar arziki ga wanda yaga dama, yana kuntatawa ga wanda yaga dama. Suna farin ciki da rayuwar duniya, rayuwar duniyabata kasance ba a cikin lahira sai ɗan amfani ƙanƙane.

28. Waɗanda suka kafirta suna faɗa "Donme ba a sauko da aya a gareshi ba, (kamar hannu da sanda da taguwa?") Cene (dasu) "Ubangiji yana ɓatar da wanda yaga damar ɓatar dashi, ayoyi baza suyi masa amfanin komai ba, yana shiriyar wanda yakoma da al'amarinsa izuwa gareshi!

FALALAR ZIKIRI DA SAKAMAKONSA)

29. Waɗannan da suka bada gaskiya, zuciyarsu take nutsuwa da ambaton Allah, to, jama'a da ambaton Allah zukata ke nutsuwa.

ثمن

ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ طُوبَىٰ لَهُمْ وَحُسْنُ مَـَٔابٍ ﴿30﴾ كَذَٰلِكَ
أَرْسَلْنَٰكَ فِيٓ أُمَّةٍ قَدْ خَلَتْ مِن قَبْلِهَآ أُمَمٌ لِّتَتْلُوَاْ عَلَيْهِمُ ٱلَّذِيٓ
أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ وَهُمْ يَكْفُرُونَ بِٱلرَّحْمَٰنِ قُلْ هُوَ رَبِّي لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ
عَلَيْهِ تَوَكَّلْتُ وَإِلَيْهِ مَتَابِ ﴿31﴾ وَلَوْ أَنَّ قُرْءَانًا سُيِّرَتْ بِهِ ٱلْجِبَالُ
أَوْ قُطِّعَتْ بِهِ ٱلْأَرْضُ أَوْ كُلِّمَ بِهِ ٱلْمَوْتَىٰ بَل لِّلَّهِ ٱلْأَمْرُ جَمِيعًا
أَفَلَمْ يَاْيْـَٔسِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَن لَّوْ يَشَآءُ ٱللَّهُ لَهَدَى ٱلنَّاسَ جَمِيعًا
وَلَا يَزَالُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ تُصِيبُهُم بِمَا صَنَعُواْ قَارِعَةٌ أَوْ تَحُلُّ
قَرِيبًا مِّن دَارِهِمْ حَتَّىٰ يَأْتِيَ وَعْدُ ٱللَّهِ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُخْلِفُ ٱلْمِيعَادَ ﴿32﴾
وَلَقَدِ ٱسْتُهْزِئَ بِرُسُلٍ مِّن قَبْلِكَ فَأَمْلَيْتُ لِلَّذِينَ كَفَرُواْ
ثُمَّ أَخَذْتُهُمْ فَكَيْفَ كَانَ عِقَابِ ﴿33﴾ أَفَمَنْ هُوَ قَآئِمٌ
عَلَىٰ كُلِّ نَفْسٍ بِمَا كَسَبَتْ وَجَعَلُواْ لِلَّهِ شُرَكَآءَ قُلْ سَمُّوهُمْ
أَمْ تُنَبِّـُٔونَهُۥ بِمَا لَا يَعْلَمُ فِي ٱلْأَرْضِ أَم بِظَٰهِرٍ مِّنَ
ٱلْقَوْلِ بَلْ زُيِّنَ لِلَّذِينَ كَفَرُواْ مَكْرُهُمْ وَصُدُّواْ عَنِ ٱلسَّبِيلِ
وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِنْ هَادٍ ﴿34﴾ لَّهُمْ عَذَابٌ فِي ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا
وَلَعَذَابُ ٱلْأٓخِرَةِ أَشَقُّ وَمَا لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ مِن وَاقٍ ﴿35﴾

30. Wadanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagari, itaciyar da ake kiranta dubata tabbata a garesu, (mahayi yana tafiya a cikin inuwarta shekara dari bai yanke ba,) da kyakkyawar makoma.

RADDI KAN MUSHIRIKAI DA BAYA-NIN IKON ALLAH A KAN KOMAI DA RARRASHI GA ANNABI SALLALLA-HU ALAIHI WASALLAMA)

31. Kamar yadda muka aiko Annabawa gabanka muka aiko ka a cikin al'umma wacce hakika al'umma suka wuce gabanta donka karanta musu abinda muka aiko izuwa gareka (alkur'ani,) su suna kafircewa da Ubangiji Arrahamanu (yayin da aka umarce su dasuyi sajada a gareshi, sukace waye Arrahamanu? Ya Annabi Muhammadu Sallallahu alaika wasallam) cene (dasu) "Allah shine Ubangijina, ba abin bautawa da gaskiya sai shi, a gareshi na dogara, izuwa gareshi nake komawa". 'Yayin da sukace dashi, in ka kasance Annabi, to, tafiyar da duwarwatsun Makka ga buranmu, ka sanya mana koramu cikintada idanduna ruwa domin mu yi dashe mu yi shuka, ka taso mana iyayenmu matattu, su ce da mu kai Annabi ne, sai Allah yace-:'
32. Da cewa ALkur'ani za a tafiyar da duwarwatsu dashi ko a keta kasa dashi, ko ayi zance da matattu dashi, (daya kasance wannan Alkur'ani ne?) Haba! al'amari na Allah ne bakibaya, (ba mai bada gaskiya sai wanda Allah yanufi imaninsa, koda an yi musu abinda suka nema. (Ubangiji ya saukar da wannan aya yayin da Sahabbai sukayi nufin bayyana abinda suka nema don kwadayi cikin imaninsu) yanzu wadanda suka bada gaskiya basu sani bada Allah yaga dama saiya shiryi mutane bakidaya (bada wata aya ba,) wadanda suka kafirta (daga mutanen Makka da waninsu) bazasu gushe masifa tana hawa kansu saboda abinda suke aikatawa (na kafirci,) ko kuma ta sauka kusa da gidaddajinsu, Makka har alkawarin Allah yazoda taimako, Ubangiji baya saba alkawari; hakika (ya sauka a Hudaibiyya ran Fatahu-Makkata.) yazo
33. Hakika an yi izgili da manzanni gabanka, (tamfar yadda akayi izgili da kai, wannan rarrashine ga Annabi Sallallahu alaihi wa-sallama,) sai nayi jinkiri ga wadanda suka kafirta, sannan na kama su da ukuba, kaka irin ukubata ta kasance? (Ta afku wurin afkuwar tao Ya Ubangiji.)

(KEWAYEWAR ALLAH DA MU DA LA'AKARINSA)

34. Yanzu wanda yake a tsaye a kan kowane mutum da abinda ya aikata, (na hairi ko sharri shine Allah, zai zama kamar wanda bai kasance kamar haka ba, na daga gumaka? A'a!) Sun sanya sharikai ga Allah, Cene, "Ku ambata mana su, su waye? Haba! kwa labarta masa da abinda bai sani ba a cikin kasa, kai! kuna ambaton su sharikaine da zahirin magana ta zato (bata hakika ba,) Bari! an kawata wa'yanda da suka kafirta kafircinsu ne, sun hana hanyar Allah, Wanda Allah ya batar dashi bashi da mai shiryarwa.
35. Azaba tana garesu a cikin rayuwar duniya (kisa da ribacewa,) azabar Lahira kuma tafi tsanani, kuma basu da masu tsarewa (daga azabar Allah.)

ربع

* مَّثَلُ اُ۬لْجَنَّةِ اِ۬لتِے وُعِدَ اَ۬لْمُتَّقُونَۖ تَجْرِے مِن تَحْتِهَا اَ۬لَانْهَٰرُۖ
أُكْلُهَا دَآئِمٞ وَظِلُّهَاۖ تِلْكَ عُقْبَى اَ۬لذِينَ اَ۪تَّقَواْۖ وَّعُقْبَى اَ۬لْكٰفِرِينَ
اَ۬لنَّارُۖ (36) وَالذِينَ ءَاتَيْنَٰهُمُ اُ۬لْكِتَٰبَ يَفْرَحُونَ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيْكَۖ
وَمِنَ اَ۬لَاحْزَابِ مَنْ يُّنكِرُ بَعْضَهُۥۖ قُلْ إِنَّمَآ أُمِرْتُ أَنَ اَعْبُدَ
اَ۬للَّهَ وَلَآ أُشْرِكَ بِهِۦٓۖ إِلَيْهِ أَدْعُواْ وَإِلَيْهِ مَـَٔابِۖ (37)
وَكَذَٰلِكَ أَنزَلْنَٰهُ حُكْماً عَرَبِيّاٗۖ وَلَئِنِ اِ۪تَّبَعْتَ أَهْوَآءَهُم
بَعْدَ مَا جَآءَكَ مِنَ اَ۬لْعِلْمِ مَا لَكَ مِنَ اَ۬للَّهِ مِنْ وَّلِيّٖ وَلَا وَاقٖۖ (38)
وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا رُسُلاٗ مِّن قَبْلِكَ وَجَعَلْنَا لَهُمُۥٓ أَزْوَٰجاٗ وَذُرِّيَّةٗۖ
وَمَا كَانَ لِرَسُولٍ اَنْ يَّأْتِيَ بِـَٔايَةٍ اِلَّا بِإِذْنِ اِ۬للَّهِۖ لِكُلِّ أَجَلٖ كِتَابٞۖ (39)
يَمْحُواْ اُ۬للَّهُ مَا يَشَآءُ وَيُثْبِتُۖ وَعِندَهُۥٓ أُمُّ اُ۬لْكِتَٰبِۖ (40) وَإِن مَّا نُرِيَنَّكَ
بَعْضَ اَ۬لذِے نَعِدُهُمْ أَوْ نَتَوَفَّيَنَّكَ فَإِنَّمَا عَلَيْكَ اَ۬لْبَلَٰغُ
وَعَلَيْنَا اَ۬لْحِسَابُۖ (41) أَوَلَمْ يَرَوَاْ أَنَّا نَأْتِي اِ۬لَارْضَ نَنقُصُهَا مِنَ
أَطْرَافِهَاۖ وَاللَّهُ يَحْكُمُ لَا مُعَقِّبَ لِحُكْمِهِۦۖ وَهُوَ سَرِيعُ اُ۬لْحِسَابِۖ (42)
وَقَدْ مَكَرَ اَ۬لذِينَ مِن قَبْلِهِمْ فَلِلَّهِ اِ۬لْمَكْرُ جَمِيعاٗۖ يَعْلَمُ
مَا تَكْسِبُ كُلُّ نَفْسٖۖ وَسَيَعْلَمُ اُ۬لْكُفْرُ لِمَنْ عُقْبَى اَ۬لدّارِۖ (43)

SIFFAR ALJANNA DA MUNAƘASHA DA MASU TA'ANNUTI DA MA'ABUTA LITTAFI DA MUSHIRIKAI)

36. Siffar aljanna wacce akayi wa masu tsoron Allah alƙawari da ita, (tana cikin abinda muke labartawa a gareku,) ƙoramu tana gudana a ƙarƙashinta, abincin ta madauwami ne, inuwar ta ma (haka, rana bata kau da ita saboda ba rana a aljanna, Wancananka aljanna Itace ƙarshen masu tsoron Allah, ƙarshen kafirai wuta.

37. Waɗanda muka basu littafi (kamar Abdullahi Ibn Salamu da waninsa,) suna farin ciki da abında aka saukar izuwa gareka (saboda daccewarsa da abinda aka saukar izuwa garesu,) akwai daga rundunar makafirta waɗanda suke musun sa shin sa (kamar ambaton (Rahmanu) Cene, "Ni an umarce ni in bautawa Allah ne kawai, kada in tara komai dashi (cikin bauta,) izuwa gareshi kaɗai nake kira, makomata ta tabbata izuwa gareshi".

38. Kamar irin wannan saukarwa ne, muka saukar da alƙur'ani, hukunci balarabe, (da luggar Larabcı daza kayi hukunci dashi tsakanin mutane.) Wallahi idan ka bi soye soyen zukatan kafirai, (taƙadiran,) bayan abinda yazo maka na ilimin tauhidi to, baka da mataimaki daga azabar Allah, wala mai hana maka azabar Allah. (Yayin da suka laifanta shi da yawan mata, sai Allah yace;)

(HUSUSIYAR KEBANTUWAR MANZON ALLAH DA YAWAN MATAYE)

39. Lalle haƙiƙa mun aiko jakadu gabanka, mun sanya musu mataye da zurriya, baza tayiwu ga manzo daga garesu ba yazoda wata aya saida izinin Allah, kowace mudda tana da littafi abar rubutawar iyakancewa a cikinsa.

40. Allah yana shafe abinda yaga dama (na hukunce - hukunce) yana tabbatar da abinda yaga dama. Uwar littafi na gareshi, (wanda ba wani abinda yake canjawa a cikinsa, shine abinda ya rubuta shi tun filazal.)

(MANZO MAI IYARWA NE, ALLAH KUMA MAI SAKAYYA NE)

41. Idan mun nuna maka ba'alin abinda muke musu alwashi dashi (na azaba a cikin rayuwarka, to, shi ke nan,) ko muka karɓi ranka (gaban bamu yi musu azaba ba,) to, ba komai a kanka sai ida aike kawai, sakamako na garemu, (zamu saka musu in sun zo gunmu.)

42. Ship mutanen Makka basayi duba ba, haƙiƙa mu, muna zuwa ƙasarsu, muna tauye ta daga gyaffanta (da buɗe ta ga Annabi Sallallahu alaihi wasallama?) Allah yana hukunta abinda yaga dama (a cikin halittarsa,) ba mai bincike ga hukuncinsa,) shine mai gaggawar sakamako.

43. Haƙiƙa waɗanda suke gabansu sun yi makirci (ga Annabawansu, tamfar yaddasulcayi makirci da kai,) to, sakamakon makircin nan yana ga Allah bakiɗaya, yasan abinda kowace kai take tsuwurwurta. Da sannu kafiri zai san gawaye kyakkyawan ƙarshe yake.

وَيَقُولُ الَّذِينَ كَفَرُواْ لَسْتَ مُرْسَلاً قُلْ كَفَىٰ بِاللَّهِ
شَهِيداَ بَيْنِي وَبَيْنَكُمْ وَمَنْ عِندَهُۥ عِلْمُ الْكِتَٰبِ ﴿44﴾

14 سُورَةُ إِبْرَٰهِيمَ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ أَرْبَعٌ وَخَمْسُونَ ءَايَةً 54

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

ثمن

* الٓرٓ كِتَٰبٌ أَنزَلْنَٰهُ إِلَيْكَ لِتُخْرِجَ النَّاسَ مِنَ الظُّلُمَٰتِ
إِلَى النُّورِ ﴿1﴾ بِإِذْنِ رَبِّهِمْ إِلَىٰ صِرَٰطِ الْعَزِيزِ الْحَمِيدِ ﴿2﴾
اللَّهُ الَّذِے لَهُۥ مَا فِي السَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ وَوَيْلٌ لِّلْكَٰفِرِينَ
مِنْ عَذَابٍ شَدِيدٍ ﴿3﴾ الَّذِينَ يَسْتَحِبُّونَ الْحَيَوٰةَ الدُّنْيَا
عَلَى ءَالَاخِرَةِ وَيَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ اللَّهِ وَيَبْغُونَهَا عِوَجاً
أُوْلَٰٓئِكَ فِي ضَلَٰلٍ بَعِيدٍ ﴿4﴾ وَمَا أَرْسَلْنَا مِن رَّسُولٍ إِلَّا
بِلِسَانِ قَوْمِهِۦ لِيُبَيِّنَ لَهُمْ فَيُضِلُّ اللَّهُ مَن يَّشَآءُ وَيَهْدِے
مَن يَّشَآءُ وَهُوَ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ ﴿5﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا مُوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَا
أَنْ أَخْرِجْ قَوْمَكَ مِنَ الظُّلُمَٰتِ إِلَى النُّورِ ﴿6﴾ وَذَكِّرْهُم بِأَيَّٰمِ اللَّهِ
إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّكُلِّ صَبَّارٍ شَكُورٍ ﴿7﴾

44. Wadanda suka kafirta suna cewa (da kai,) "Baka kasance manzo ba", Cene (dasu) "Allah ya isa shaida tsakanina daku ,(bisa gaskiyata,) da wanda ilimin littafi yake gareshi, (sune muminan Yahudu da Nasara.)

Suratu Ibrahima Alaihissalam

A Makka Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Hamsin Da Hudu (54)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabadaya, mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

'Ita wannan sura tayi zance a kan ayoyi na kaunu, da tabbatar da tashin alƙiyama da saba misalce-misalce ga ƙarya da gaskiya da makircin kafirai da aƙiba tasa.'

(NI'IMAR SAUKAR DA ALƘUR'ANI DA SAUKAR DA MANZO DATASIRINSU)

1.A.L.R. (Allah ne masani da abinda yake nufi da wannan kalma,) Wannan Alƙur'ani littafi ne da' muka saukar dashi a gareka, ya (Annabi Sallallahu alaika wasallama,) donka fitar da mutane daga duffan kafirci izuwa hasken (imani.)
2. Da umarnin Ubangijinsu izuwa tafarkin mai rinjaye abin godewa.
3. Sarki Allah, wanda mulkin sammai da ƙassaiya tabbata a gareshi (mallaka da halittada bauta,) zazan azabaya tabbata ga kafirai, na azaba mai tsanani.
4. Wadannan dasuke fifita rayuwar duniya a kan lahira suke hana mutane bin addinin Allah, suke neman wannan tafarki halin kasancewar ta a karkace, wadancananka suna cikin bata mai nisa (ga buran gaskiya.)
5. Bamu aiko wani manzo ba face dayaren mutanensa, domin ya bayyana musu abinda yazo dashi, shi Ubangiji yana ɓatar da wanda yaga dama yana shiriyar wanda yaga dama, shine mabuwayi (cikin mulkinsa) gwani (cikin aikinsa.)

(BABBAN AIKIN MANZANNI ALAIHIMUSSALAM)

6. Haƙiƙa mun aiko Annabi Musa Alaihissalam da ayoyi (guda tara, mun ce dashi) "Fitar da mutanenka daga duffan (kafirci) izuwa hasken imani.
7. "Ka gargadar dasu dani ,imomin Ubangiji, haƙiƙa cikin wancananka akwai ayoyi ga dukkan mai dauriya (a kan da'a,) mai yawan godiya (ga ni'imomin Allah".)

وَإِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِقَوْمِهِ اذْكُرُوا نِعْمَةَ اللَّهِ عَلَيْكُمْ
إِذْ أَنجَاكُم مِّنْ ءَالِ فِرْعَوْنَ يَسُومُونَكُمْ سُوٓءَ الْعَذَابِ
وَيُذَبِّحُونَ أَبْنَآءَكُمْ وَيَسْتَحْيُونَ نِسَآءَكُمْ وَفِي ذَٰلِكُم
بَلَآءٌ مِّن رَّبِّكُمْ عَظِيمٌ ﴿8﴾ وَإِذْ تَأَذَّنَ رَبُّكُمْ لَئِن شَكَرْتُمْ
لَأَزِيدَنَّكُمْ وَلَئِن كَفَرْتُمْ إِنَّ عَذَابِي لَشَدِيدٌ ﴿9﴾ وَقَالَ مُوسَىٰ
إِن تَكْفُرُوا أَنتُمْ وَمَن فِي الْأَرْضِ جَمِيعًا فَإِنَّ اللَّهَ لَغَنِيٌّ حَمِيدٌ ﴿10﴾
أَلَمْ يَأْتِكُمْ نَبَؤُا الَّذِينَ مِن قَبْلِكُمْ قَوْمِ نُوحٍ وَعَادٍ
وَثَمُودَ ﴿11﴾ وَالَّذِينَ مِنۢ بَعْدِهِمْ لَا يَعْلَمُهُمْ إِلَّا اللَّهُ جَآءَتْهُمْ
رُسُلُهُم بِالْبَيِّنَاتِ فَرَدُّوا أَيْدِيَهُمْ فِي أَفْوَاهِهِمْ
وَقَالُوا إِنَّا كَفَرْنَا بِمَا أُرْسِلْتُم بِهِ وَإِنَّا لَفِي شَكٍّ مِّمَّا
تَدْعُونَنَا إِلَيْهِ مُرِيبٍ ﴿12﴾ * قَالَتْ رُسُلُهُمْ أَفِي اللَّهِ شَكٌّ
فَاطِرِ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ يَدْعُوكُمْ لِيَغْفِرَ لَكُم
مِّن ذُنُوبِكُمْ وَيُؤَخِّرَكُمْ إِلَىٰ أَجَلٍ مُّسَمًّى قَالُوا إِنْ
أَنتُمْ إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُنَا تُرِيدُونَ أَن تَصُدُّونَا عَمَّا
كَانَ يَعْبُدُ ءَابَآؤُنَا فَأْتُونَا بِسُلْطَانٍ مُّبِينٍ ﴿13﴾

ربع

8. Ka ambata zamanin da Annabi Musa (Alaihissalam yake faɗa ga mutanensa,) "Ku ambaci ni'imomin Allah gareku donya tserar daku ,daga mutanen Fir'auna, suna ɗanɗana muku mummunar azaba, suna yanyan-ka "ya"yayenku (waɗanda aka haifa,) suna raya matayenku, (saboda faɗin ba'alin bokaye "Haƙiƙa wani abin haihuwa za a haife shi cikin Bani-Isra'ila, zai kasance sababin tafiyar mulkin Fir'auna,") a cikin wancananku (tserarwa ko azabtarwa,) akwai bala'i mai girma daga Ubangijinku".
9. Ka ambata zamanin da Ubangijinku yasanar lalle idan kun godewa ni'imata (da tauhidi da da'a,) Wallahi zan ƙara muku,Wallahi in kun kafirce, haƙiƙa azabata mai tsanani ce.
10. Annabi Musa (Alaihissalam ya faɗa ga mutanensa,) in kun kafirta kuda wanda yake cikin ƙasa bakiɗaya, to, haƙiƙa Ubangiji mawadaci ne (ga buran halitta tasa) abin godewa ne (a cikin aikinsa dayayi dasu.)

BA'ALIN LABARAN AL'UMMA MARIGAYIYA)

11. Shin labaran waɗanda suke ga-banku basu zo muku ba ne? Mutanen Annabi Nuhu da Adu da Samudu.
12. Da waɗanda suke bayansu ba wanda yasan su sai Allah (saboda yawansu,) manzanninsu sun zo musu da hujjoji mabayyana (saboda gaskiyarsu,) sai suka maida hannuwansu cikin bakunansu (donsu ciji "yan yat-sunsu don tsananin fushi) sukace mu, "Mun kafirtada abinda aka aikoku dashi, haƙiƙa mu lalle muna cikin kokwanto daga abinda kuke kiranmu izuwa gareshi kokwanto mai afkarwa a cikin tuhuma".

(DALILI BISA SAMUWAR ALLAH) NUSUFI

13. Manzanninsu sukace (dasu) akwai kokwanto a cikin samuwar Allah? (Babu.) Mahaliccin sammai da ƙassai, yana kiranku (izuwa ɗa'a) donya gafarta muku zunubanku, yajinkirta muku azaba izuwa ajali abin ambato, (mutuwa,) Sukace, "Ku, baku kasance ba sai mutane tamkar mu, kuna nufin ku hana mu ga buran abinda iyayenmu suke bautawa (na daga gumaka,) kuzo mana da hujja mabayyaniya (a bisa gaskiyarku.)

قَالَتْ لَهُمْ رُسُلُهُمْ إِن نَّحْنُ إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ وَلَٰكِنَّ اللَّهَ يَمُنُّ عَلَىٰ
مَن يَشَاءُ مِنْ عِبَادِهِۦ وَمَا كَانَ لَنَا أَن نَّأْتِيَكُم بِسُلْطَٰنٍ
إِلَّا بِإِذْنِ اللَّهِ وَعَلَى اللَّهِ فَلْيَتَوَكَّلِ الْمُؤْمِنُونَ ﴿14﴾
وَمَا لَنَا أَلَّا نَتَوَكَّلَ عَلَى اللَّهِ وَقَدْ هَدَىٰنَا سُبُلَنَا وَلَنَصْبِرَنَّ
عَلَىٰ مَا ءَاذَيْتُمُونَا وَعَلَى اللَّهِ فَلْيَتَوَكَّلِ الْمُتَوَكِّلُونَ ﴿15﴾
وَقَالَ الَّذِينَ كَفَرُوا لِرُسُلِهِمْ لَنُخْرِجَنَّكُم مِّنْ أَرْضِنَا
أَوْ لَتَعُودُنَّ فِي مِلَّتِنَا فَأَوْحَىٰ إِلَيْهِمْ رَبُّهُمْ لَنُهْلِكَنَّ
الظَّٰلِمِينَ ﴿16﴾ وَلَنُسْكِنَنَّكُمُ الْأَرْضَ مِنْ بَعْدِهِمْ
ذَٰلِكَ لِمَنْ خَافَ مَقَامِي وَخَافَ وَعِيدِ ﴿17﴾ وَاسْتَفْتَحُوا
وَخَابَ كُلُّ جَبَّارٍ عَنِيدٍ ﴿18﴾ مِّن وَرَآئِهِۦ جَهَنَّمُ وَيُسْقَىٰ
مِن مَّآءٍ صَدِيدٍ ﴿19﴾ يَتَجَرَّعُهُۥ وَلَا يَكَادُ يُسِيغُهُۥ وَيَأْتِيهِ
الْمَوْتُ مِن كُلِّ مَكَانٍ وَمَا هُوَ بِمَيِّتٍ وَمِن وَرَآئِهِۦ
عَذَابٌ غَلِيظٌ ﴿20﴾ مَّثَلُ الَّذِينَ كَفَرُوا بِرَبِّهِمْ أَعْمَٰلُهُمْ
كَرَمَادٍ اشْتَدَّتْ بِهِ الرِّيَاحُ فِي يَوْمٍ عَاصِفٍ لَّا يَقْدِرُونَ
مِمَّا كَسَبُوا عَلَىٰ شَيْءٍ ذَٰلِكَ هُوَ الضَّلَٰلُ الْبَعِيدُ ﴿21﴾

14. Sai manzannin sukace (dasu,) "Mu, bamu kasance ba face mutane kamar ku (tamfar yadda kuka faɗa,) sai dai Allah yana yin baiwa (da Annabci) bisa wanda yaga dama daga bayinsa, bai kamata a garemu mu zo mukuda hujja ba, saida izinin Allah, (don mu bayi ne ababan mallaka,) to, bisa ga Allah dukkan muminai suke dogara.
15. "Meke garemu da bazamu dogara ga Allah ba, haƙiƙa ya shirye mu tafarkunmu, lalle zamu haƙura bisa cutar da kukayi mana, to, a bisa Allah kawai muminai su dogara".

(KYAKKYAWAN ƘARSHE YA TABBATA GA MASU TSORON ALLAH)

16. Waɗanda suka kafirta suka faɗa ga manzanninsu, "Lalle zamu fitar daku ,daga ƙasarmu, ko lalle ku zama a cikin addininmu," Sai Allah ya aiko izuwa garesu, "Lalle zamu halakar da kafirai.
17. "Lalle zamu zaunar daku ,ƙasassu bayan halakarsu, wancananka (nasara da gadon kasa,) yana ga wanda yaji tsoron tsaiwa gabana, yaji tsoron azabata.
18. Jakadu sun nemi taimako da Allah (a kan mutanensu,) dukkan mai taurin kai mai kin gaskiyaya taɓe.
19. Jahannama na gabansa (zai shigeta,) za a shayar dashi daga cikinta daga ruwa na surkami.
20. Yana kwankwaɗa tasa (lokaci bayan lokaci saboda dacinsa, bazai kusa ya hadiye shi ba, saboda munin sa da kyamarsa,) sabubban mutuwa zasu kewaye dashi daga kowane wuri, shi bazai mutu ba (balle ya huta,) bay-ansa akwai azaba mai kauri.

AYYUKA NAGARI NA KAFIRAI BASU DA AMFANI A LAHIRA)

21. Siffar waɗanda suka kafirtada Ubangijinsu ayyukansu nagari, (sadar da zumuntada sadaka, a cikin rashin amfanuwa da ita,) kamar tokace iska ta tsanantada ita a rana mai tsananin guguwa, basu da iko a kan wani abu daga abinda suka aikata (a duniya, bazasu sami sakamakonsa ba saboda rashin sharaɗinsa, wato Musulunci,) Wancananka shine ɓata mai nisa (ga buran gaskiya.)

ثمن

أَلَمْ تَرَ أَنَّ اللَّهَ خَلَقَ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضَ بِالْحَقِّ إِن يَشَأْ
يُذْهِبْكُمْ وَيَأْتِ بِخَلْقٍ جَدِيدٍ ﴿22﴾ وَمَا ذَٰلِكَ عَلَى اللَّهِ بِعَزِيزٍ ﴿23﴾
وَبَرَزُوا لِلَّهِ جَمِيعًا فَقَالَ الضُّعَفَاءُ لِلَّذِينَ اسْتَكْبَرُوا إِنَّا كُنَّا
لَكُمْ تَبَعًا فَهَلْ أَنتُم مُّغْنُونَ عَنَّا مِنْ عَذَابِ اللَّهِ مِن شَيْءٍ
قَالُوا لَوْ هَدَانَا اللَّهُ لَهَدَيْنَاكُمْ سَوَاءٌ عَلَيْنَا أَجَزِعْنَا أَمْ صَبَرْنَا
مَا لَنَا مِن مَّحِيصٍ ﴿24﴾ وَقَالَ الشَّيْطَانُ لَمَّا قُضِيَ الْأَمْرُ
إِنَّ اللَّهَ وَعَدَكُمْ وَعْدَ الْحَقِّ وَوَعَدتُّكُمْ
فَأَخْلَفْتُكُمْ وَمَا كَانَ لِيَ عَلَيْكُم مِّن سُلْطَانٍ
إِلَّا أَن دَعَوْتُكُمْ فَاسْتَجَبْتُمْ لِي فَلَا تَلُومُونِي وَلُومُوا أَنفُسَكُم
مَّا أَنَا بِمُصْرِخِكُمْ وَمَا أَنتُم بِمُصْرِخِيَّ إِنِّي كَفَرْتُ بِمَا
أَشْرَكْتُمُونِ مِن قَبْلُ إِنَّ الظَّالِمِينَ لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿25﴾
وَأُدْخِلَ الَّذِينَ آمَنُوا وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ جَنَّاتٍ تَجْرِي
مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَارُ خَالِدِينَ فِيهَا بِإِذْنِ رَبِّهِمْ تَحِيَّتُهُمْ
فِيهَا سَلَامٌ ﴿26﴾ أَلَمْ تَرَ كَيْفَ ضَرَبَ اللَّهُ مَثَلًا كَلِمَةً طَيِّبَةً
كَشَجَرَةٍ طَيِّبَةٍ أَصْلُهَا ثَابِتٌ وَفَرْعُهَا فِي السَّمَاءِ

ARUSHE,SHENIYAR MAGANA TSAK-ANIN "YAN WUTA NA DAGA RAU-NANA DA MANYA DA SHAIDAN)

22. Shin baka duba, haƙiƙa Ubangiji ya halicci sammai da ƙassaida gaskiya, in yaga dama saiya tafi daku ,(Yaku mutane) yazoda halitta sabuwa (maimakon ku,) wannan ba mai wahalarwa ne ba bisa Allah.
23. Halitta zasu fita ga Allah bakiɗaya, sai mabiya su faɗa ga shiyagabanninsu, "Haƙiƙa mu, mun kasance mabiyagareku, Shin ku, ba kwa ije mana wani abu na daga azabar Allah ba?" Su shiyagabannin sukace (dasu,) "Da Allah ya shirye mu da sai mu shiryeku, rakinmu, ko dauriyarmu duk daya ne garemu, bamu da wata makarɗaɗa".
24. Sai Iblis ya fadayayin da aka hukunta shiga aljanna ga "yan aljanna, dashiga wuta ga 'yan wuta, (suka tattara gareshi, yace,) " Haƙiƙa Ubangiji yayi muku alkwari, alƙawarin gaskiya, (ya gasgata muku alƙawari,) ni kuma nayi muku alƙawari na ƙarya, na saba muku, to, ba wani karfi da nake dashi a kanku, sai dai na kirawo kune kuka amsa min, kadaku ,zarge ni, ku zargi kanku, ni, ba mai taimakonku ba ne, ku ba masu taimakona ne ba, haƙiƙa ni, na kafirta dashirkanta ni da kukayi tareda Allah tun gaba (a duniya", Ubangiji yace,) "Haƙiƙa kafirai azaba mai raɗaɗi ta tabbata a garesu".
25. Aka shigar da waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagari, aljannatai wacce ƙoramu take gudana a ƙarƙashinta;masu dauwama a cikintada izinin Ubangijinsu, gaisuwarsu a cikinta daga Allah da Mala'ikuda tsakaninsu, lafazin SALAMU.

(FALALAR LA-ILAHA ILLALLAHU DA KISHIYARTA)

26. Baka duba yaya Ubangiji yasanya misali kalma daddaɗa (La'ilahaillallahu,) kamar itaciyace daddaɗa, (dabinuwa,) asalinta yana tabbace a cikin ƙasa, reshenta yana sama.
27. Tana bada amfaninta a kowane lokaci da iznin Ubangijinta, (yana nufin kalmar imani tabbatacciyace a cikin zuciyar mumi-nai, aikinsa yana hawa izuwa sama, yana samun albarkar aikinsa a kowane lokaci,) Allah yana bayyana misalce-misalce ga mutane donsu wa'azantu. (Sawitun daga nan ne Sufaye suka keɓantada ita, suka karɓe ta ga shehunansu da sanadi sajajje, suka ɗanfare mata har ta zama rigarsu da taguwarsu, don haka shehu Sunusi AlTulumsani yace, Ya wajaba ga mai hankali ya yawaita daga ambatonta, yana halartarwa ga abindata ƙunsa na daga ma'anoni har ta cudanya tareda ma'anartada namansa da jininsa, haƙiƙa shi zai gani daga gareta na daga abinda bazai shiga ƙarƙashin tsarewa bana daga asirai da mana kai.)

تُؤْتِےٓ أُكْلَهَا كُلَّ حِينِۢ بِإِذْنِ رَبِّهَاۖ وَيَضْرِبُ اُ۬للَّهُ اُ۬لْأَمْثَالَ
لِلنَّاسِ لَعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَۖ ﴿27﴾ وَمَثَلُ كَلِمَةٍ خَبِيثَةٍ كَشَجَرَةٍ
خَبِيثَةٍ اِ۪جْتُثَّتْ مِن فَوْقِ اِ۬لْأَرْضِ مَا لَهَا مِن قَرَارٖۖ ﴿28﴾
يُثَبِّتُ اُ۬للَّهُ اُ۬لذِينَ ءَامَنُواْ بِالْقَوْلِ اِ۬لثَّابِتِ فِے اِ۬لْحَيَوٰةِ اِ۬لدُّنْيَا
وَفِے اِ۬لْأٓخِرَةِۖ وَيُضِلُّ اُ۬للَّهُ اُ۬لظَّٰلِمِينَۖ وَيَفْعَلُ اُ۬للَّهُ مَا يَشَآءُۖ ﴿29﴾

* أَلَمْ تَرَ إِلَى اَ۬لذِينَ بَدَّلُواْ نِعْمَتَ اَ۬للَّهِ كُفْراً
وَأَحَلُّواْ قَوْمَهُمْ دَارَ اَ۬لْبَوَارِ ﴿30﴾ جَهَنَّمَ يَصْلَوْنَهَاۖ وَبِيسَ
اَ۬لْقَرَارُۖ ﴿31﴾ وَجَعَلُواْ لِلهِ أَندَاداً لِّيُضِلُّواْ عَن سَبِيلِهِۦۖ
قُلْ تَمَتَّعُواْ فَإِنَّ مَصِيرَكُمْ إِلَى اَ۬لنَّارِۖ ﴿32﴾ قُل لِّعِبَادِيَ اَ۬لذِينَ
ءَامَنُواْ يُقِيمُواْ اُ۬لصَّلَوٰةَ وَيُنفِقُواْ مِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ سِرّاً وَعَلَانِيَةً
مِّن قَبْلِ أَن يَّأْتِيَ يَوْمٌ لَّا بَيْعٌ فِيهِ وَلَا خِلَٰلٌۖ ﴿33﴾ اُ۬للَّهُ اُ۬لذِے
خَلَقَ اَ۬لسَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضَ وَأَنزَلَ مِنَ اَ۬لسَّمَآءِ مَآءً فَأَخْرَجَ
بِهِۦ مِنَ اَ۬لثَّمَرَٰتِ رِزْقاً لَّكُمْۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ اُ۬لْفُلْكَ لِتَجْرِيَ
فِے اِ۬لْبَحْرِ بِأَمْرِهِۦۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ اُ۬لْأَنْهَٰرَۖ ﴿34﴾ وَسَخَّرَ لَكُمُ
اُ۬لشَّمْسَ وَالْقَمَرَ دَآئِبَيْنِۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ اُ۬ليْلَ وَالنَّهَارَۖ ﴿35﴾

28. Misalin kalma mummuna (kalmar kafirci, wato dukkan kalmar da Musulmi zaiyi ridda sa-boda ita) kamar itaciyace mummuna (guna) aka tunɓuke ta daga birbishin kasa, matabbaci bai kasance gareta ba, (batada reshe batada albarka.)

(TAMBAYON MALA'IKKU A CIKIN KABARI)

29. Allah yana tabbatar da waɗanda suka bada gaskiya da magana tabbatacciya, (kalmar Tauhidi,) a cikin rayuwar duniya data lahira, a cikin ƙabari (yayin da Mala'iku guda biyu suke tambayonsu ga Ubangijinsu da addininsu da Annabinsu, su amsa da jawabi madaidaici, kamar da Buhari da Muslim suka faɗa,) Allah yana ɓatar da kafirai, bazasu shiriya izuwa jawabi mai dacewa ba, saisu ce bamu sani ba, tamfar dayazo cikin Hadisi, Allah yana aikata abinda yaga dama, ba mai bincike ga hukuncinsa.

(BARAZANA DA AIKIN KAFIRCI DA KWADAITARWA KAN TSAYAR DA SALLA DA AIKATA ALHERI)

30. Shin bakayi duba ba izuwa waɗannan da suka misanya ni'ima da kafirci, suka saukar da mutanensu gidan halaka?
31. Jahannama suna shigarta, tir! matabbaci ita.
32. Sun sanya sharikai ga Allah, donsu ɓatar ga buran addinin Musulunci, Cene (dasu) kuji daɗi a duniyarku kaɗan, haƙiƙa makomar ku izuwa wuta ne.
33. Cene da bayina waɗanda suka bada gaskiya, su tsayar da salla, su ciyar daga abinda muka azurta musu a asirce da bayyane, tun gaban rana wacce ba fansa cikinta, bakawance, batazo ba, (ranar Alƙiyama.)

(IN KUN ƘIDAYA NFIMAR ALLAH BAZAKU KEWAYE DA ITA BA)

34. Allah ne wanda ya halicci sammai da ƙassai, ya saukar da ruwa daga sama, yafitar dashi daga nau'in itatuwa, don azurta wa gareku, ya hore maku jiraga donta gudana a cikin kogi da iznin Allah, ya hore muku ƙoramu.
35. Ya hore muku rana da wata, masu gudu a cikin falakinsu tutur, ya hore muku dare don ku nutsu ciki, da rana don ku nema daga arzikinsa.

وَءَاتَىٰكُم مِّن كُلِّ مَا سَأَلْتُمُوهُ وَإِن تَعُدُّواْ نِعْمَتَ ٱللَّهِ لَا تُحْصُوهَآ
إِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ لَظَلُومٌ كَفَّارٌ ﴿36﴾ وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِيمُ
رَبِّ ٱجْعَلْ هَٰذَا ٱلْبَلَدَ ءَامِناً وَٱجْنُبْنِي وَبَنِيَّ أَن نَّعْبُدَ
ٱلْأَصْنَامَ ﴿37﴾ رَبِّ إِنَّهُنَّ أَضْلَلْنَ كَثِيراً مِّنَ ٱلنَّاسِ
فَمَن تَبِعَنِي فَإِنَّهُۥ مِنِّي وَمَنْ عَصَانِي فَإِنَّكَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿38﴾
رَّبَّنَا إِنِّي أَسْكَنتُ مِن ذُرِّيَّتِي بِوَادٍ غَيْرِ ذِي زَرْعٍ
عِندَ بَيْتِكَ ٱلْمُحَرَّمِ رَبَّنَا لِيُقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ فَٱجْعَلْ أَفْئِدَةً مِّنَ
ٱلنَّاسِ تَهْوِي إِلَيْهِمْ وَٱرْزُقْهُم مِّنَ ٱلثَّمَرَٰتِ لَعَلَّهُمْ يَشْكُرُونَ ﴿39﴾
رَبَّنَا إِنَّكَ تَعْلَمُ مَا نُخْفِي وَمَا نُعْلِنُ وَمَا يَخْفَىٰ عَلَى ٱللَّهِ
مِن شَيْءٍ فِي ٱلْأَرْضِ وَلَا فِي ٱلسَّمَآءِ ﴿40﴾ ۞ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ
ٱلَّذِي وَهَبَ لِي عَلَى ٱلْكِبَرِ إِسْمَٰعِيلَ وَإِسْحَٰقَ إِنَّ رَبِّي
لَسَمِيعُ ٱلدُّعَآءِ ﴿41﴾ رَبِّ ٱجْعَلْنِي مُقِيمَ ٱلصَّلَوٰةِ وَمِن ذُرِّيَّتِي
رَبَّنَا وَتَقَبَّلْ دُعَآءِ ﴿42﴾ رَبَّنَا ٱغْفِرْ لِي وَلِوَٰلِدَيَّ وَلِلْمُؤْمِنِينَ
يَوْمَ يَقُومُ ٱلْحِسَابُ ﴿43﴾ وَلَا تَحْسِبَنَّ ٱللَّهَ غَٰفِلاً عَمَّا يَعْمَلُ
ٱلظَّٰلِمُونَ إِنَّمَا يُؤَخِّرُهُمْ لِيَوْمٍ تَشْخَصُ فِيهِ ٱلْأَبْصَٰرُ ﴿44﴾

ثمن

36. Ya baku daga dukkan abinda kuka roƙe shi (gwargwadon masalahohinku,) in kun ƙirga ni'imar Allah bazaku iya kewayewa da ita ba, haƙiƙa shi kafiri mai yawan zalunta ne ga kansa (da saɓo,) mai yawan butulci ne (da ni'imar Ubangijin-sa.)

(ADDU,AR ANNABI IBRAHIM ALAIHISSALAM)

37. Ambaci zamanin da Annabi Ibrahim (Alaihiassalam) yace, "Ubangiji! sanya wannan gari (Makka) amintacce, (Allah kuwa ya amsa addu'ar, Ya sanyashi harami ba'zub'da jinin mutun acikinsa ba a zaluntar kowa a cikinsa, ba a farautar namansa, ba a yankan ciyawarsa,) ka nisanta ni dani da "ya"yana ga buran bautar gumaka.

38. "Ubangiji! haƙiƙa su gumaka sun ɓatar da yawaici daga mu-tane, wanda ya bini (a kan tauhidi,) to, haƙiƙa shi daga gareni yake, (daga masu addinina,) wanda ya sabe imi kuwa haƙiƙa kai mai gafara ne mai jinƙai, (wannan gaban saninsa ne cewa Allah baya gafarta shirka.)

39. "Ya Ubangijinmu, haƙiƙa m na zaunar da zurriyata (annabi Isma'ila da mahaifiyarsa Hajaru Alaihimussalamu,) a zaza ba mai shuka bashine Makka nan ga Dakinka mai alfarma (wanda ya kasance gaban dufanu,) Ya Ubangijinmu! domin su tsayar da salla, ka sanya zukata daga mutane ta dinga karkata izuwa garesu, (Ibn Abbasu yace, dayace zukatan mutane da Farisa da Rome da duk mutanen duniya dasun yi bege izuwa gareshi,) Ka azurta su daga "ya" yan itaciya saboda su suyi ma godiya, (ya aikata wannan da ciro ɗa'ifa izuwa gareshi a da, a yanzu kuma da ɓarke duniya ta kowace al'umma takai albarkatan ƙasar ta izuwa gareshi, da fitar da ma'adinai; baramu na arzuka da fetur).

40. "Ubangijinmu! Kaine kasan abinda muke ɓoyewa da abinda muke bayyanawa, babu daga wani abu da yake ɓuyaga Allah a cikin ƙassai ko a cikin sammai.

41. "Godiya ta tabbata ga Ubangiji wanda ya bani Annabi Isma'ila (Alaihissalam) tareda tsufa (ina ɗan shekara ɗari ɗayababu,) da Annabi Ishaƙu (Alaihissalam, ina dan shekara dari da goma sha biyu,) haƙiƙa Ubangijina maji roƙo ne.

42. "Ubangijina! Sanya ni mai tsayar da salla, ka sanya kuma daga cikin zuriyyata wandazai tsayar da ita. (An amsa masa wannan da Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama,) Ya Ubangijinmu! ka karɓi adu'a ta wacce na ambata.

43. "Ubangijinmu! Yi gafara gareni da iyayena, (ya nuna cewa iyayensa da sukayi mubasharar halihuwarsa Musulmi ne) kuma kayi ga muminai ranar da hisabi yake tabbata".

(GARGADI DA RANAR ALƘIYAMA DA MATSAYANTA)

44. Kadaka zaci Ubangiji marabkanine ga abinda kafirai suke aikatawa, haƙiƙa yana jinkirta musune izuwa rana wadda idanuwa take fitowa zuruzuru.

مُهْطِعِينَ مُقْنِعِي رُءُوسِهِمْ لَا يَرْتَدُّ إِلَيْهِمْ طَرْفُهُمْ
وَأَفْئِدَتُهُمْ هَوَاءٌ ﴿45﴾ وَأَنذِرِ النَّاسَ يَوْمَ يَأْتِيهِمُ الْعَذَابُ
فَيَقُولُ الَّذِينَ ظَلَمُوا رَبَّنَا أَخِّرْنَا إِلَىٰ أَجَلٍ قَرِيبٍ نُّجِبْ
دَعْوَتَكَ وَنَتَّبِعِ الرُّسُلَ أَوَلَمْ تَكُونُوا أَقْسَمْتُم مِّن قَبْلُ
مَا لَكُم مِّن زَوَالٍ ﴿46﴾ وَسَكَنتُمْ فِي مَسَاكِنِ الَّذِينَ
ظَلَمُوا أَنفُسَهُمْ وَتَبَيَّنَ لَكُمْ كَيْفَ فَعَلْنَا بِهِمْ وَضَرَبْنَا
لَكُمُ الْأَمْثَالَ ﴿47﴾ وَقَدْ مَكَرُوا مَكْرَهُمْ وَعِندَ اللَّهِ
مَكْرُهُمْ وَإِن كَانَ مَكْرُهُمْ لِتَزُولَ مِنْهُ
الْجِبَالُ ﴿48﴾ فَلَا تَحْسِبَنَّ اللَّهَ مُخْلِفَ وَعْدِهِ رُسُلَهُ
إِنَّ اللَّهَ عَزِيزٌ ذُو انتِقَامٍ ﴿49﴾ يَوْمَ تُبَدَّلُ الْأَرْضُ غَيْرَ الْأَرْضِ
وَالسَّمَاوَاتُ وَبَرَزُوا لِلَّهِ الْوَاحِدِ الْقَهَّارِ ﴿50﴾ وَتَرَى الْمُجْرِمِينَ
يَوْمَئِذٍ مُّقَرَّنِينَ فِي الْأَصْفَادِ ﴿51﴾ سَرَابِيلُهُم مِّن قَطِرَانٍ وَتَغْشَىٰ
وُجُوهَهُمُ النَّارُ ﴿52﴾ لِيَجْزِيَ اللَّهُ كُلَّ نَفْسٍ مَّا كَسَبَتْ
إِنَّ اللَّهَ سَرِيعُ الْحِسَابِ ﴿53﴾ هَٰذَا بَلَاغٌ لِّلنَّاسِ وَلِيُنذَرُوا بِهِ
وَلِيَعْلَمُوا أَنَّمَا هُوَ إِلَٰهٌ وَاحِدٌ وَلِيَذَّكَّرَ أُولُو الْأَلْبَابِ ﴿54﴾

45. Masu gaggawa, masu ɗaga kawukansu izuwa sama, ganinsu ba yakomowa izuwa garesu, zukatansu mawofunta ne ga buran hankula.
46. Tsoratar da miitane (Ya Annabi Muhammadu Sallalahu alaika wasallama,) ranar da azabaza tazo musu, waɗanda sukayi zalunci su ce "Ya Ubangijinmu! jinkirta mana (da mayar da mu izuwa duniya,) izuwa ajali makusanci, mu amsa kiranka (na tauhidi,) mu bi manzanninka, (sai a ce dasu don kuruztawa,) "Baku kasance kun rantse bane tun gaba (a duniya,) bakuda kawa (ga buranta izuwa Lahira!)
47. "Kun zauna a duniya a mazaunin waɗanda suka zalunci kansu (na daga al'ummai da suka rigaya,) kun ga yadda muka aikata dasu (baku tsautu ba,) mun bayyana muku misalce misalce (cikin alƙur'ani, bakuyi izna ba.)

(MAKIRCIN KAFIRAI GA MA'AIKI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA DA TABBATAR SHARFAR MUSULUNCI)

48. Haƙiƙa sun yi makirci (da Annabi Sallallahu alaihi wasallama irin makircinsu, kashe shi ko ɗaure shi, ko fitar dashi,) sakamakon kafircinsu na ga Allah, makircinsu bai kasance duwarwatsu sli gushe saboda shi ba, (wato shari'o'in Musulunci.)
49. Kadaka zaci Ubangiji zai saɓawa manzanninsa alƙawarinsa (da taimako,) haƙiƙa Ubangiji mabuwayi ne mai ban kashine (ga wanda ya saɓe shi.)
50. Ambaci ranar da ake musanya kasada, wata ƙasa ba wannan da muke kaiba, ake musanya sammai (shine ranar alƙiyama,) a tara mutane a kan ƙasa fara fat (tamfar dayazo cikin Buhari da Muslim, An tambayi Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama, mutane suna ina a wannan lokaci yace suna kan siraɗi) sun fito daga ƙaburbura ga Allah makadaici mai yawan rinjaye.
51. Kana ganin masu laifi a wannan rana ababan ɗaurewa (tareda shaiɗanunsu a cikin maruruwa ?
52. Rigunansu na man gelo ne, wuta tana lulluɓe fuskokinsu.
53. Sun fito daga ƙaburbura saboda Allah ya sakawa kowace kai abindata aikata (na hairi ko sharri,) haƙiƙa Allah mai gaggawar sakamako ne, (zai gama hisabi cikin rabin rana na kwanukan duniya.)
54. Wannan alƙur'ani iyarwa ne ga mutane (an saukar dashi) donya iyar musu, donsu tsoratar dashi kuma donsu san (abinda yake cikinsa na hujjoji,) haƙiƙa Ubangiji, Ubangiji ne makaɗaici kawai! Saboda kuma ma'abuta hankula su wa'azantu.

حزب

15 سُورَةُ الْحِجْرِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ تِسْعٌ وَتِسْعُونَ ءَايَةً 99

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

* الٓر تِلْكَ ءَايَٰتُ الْكِتَٰبِ وَقُرْءَانٍ مُّبِينٍ ﴿1﴾ رُبَمَا يَوَدُّ الَّذِينَ
كَفَرُواْ لَوْ كَانُواْ مُسْلِمِينَ ﴿2﴾ ذَرْهُمْ يَأْكُلُواْ وَيَتَمَتَّعُواْ وَيُلْهِهِمُ
الْأَمَلُ فَسَوْفَ يَعْلَمُونَ ﴿3﴾ وَمَا أَهْلَكْنَا مِن قَرْيَةٍ اِلَّا وَلَهَا كِتَابٌ
مَّعْلُومٌ ﴿4﴾ مَّا تَسْبِقُ مِنْ اُمَّةٍ اَجَلَهَا وَمَا يَسْتَأْخِرُونَ ﴿5﴾ وَقَالُواْ
يَٰأَيُّهَا الَّذِي نُزِّلَ عَلَيْهِ الذِّكْرُ إِنَّكَ لَمَجْنُونٌ ﴿6﴾ لَّوْمَا تَأْتِينَا
بِالْمَلَٰٓئِكَةِ إِن كُنتَ مِنَ الصَّٰدِقِينَ ﴿7﴾ مَا تَنَزَّلُ الْمَلَٰٓئِكَةُ
إِلَّا بِالْحَقِّ وَمَا كَانُواْ إِذاً مُّنظَرِينَ ﴿8﴾ إِنَّا نَحْنُ نَزَّلْنَا الذِّكْرَ
وَإِنَّا لَهُ لَحَٰفِظُونَ ﴿9﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ فِي شِيَعِ الْأَوَّلِينَ ﴿10﴾
وَمَا يَأْتِيهِم مِّن رَّسُولٍ اِلَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿11﴾ كَذَٰلِكَ نَسْلُكُهُۥ
فِي قُلُوبِ الْمُجْرِمِينَ ﴿12﴾ لَا يُؤْمِنُونَ بِهِۦ وَقَدْ خَلَتْ سُنَّةُ الْأَوَّلِينَ ﴿13﴾
وَلَوْ فَتَحْنَا عَلَيْهِم بَاباً مِّنَ السَّمَآءِ فَظَلُّواْ فِيهِ يَعْرُجُونَ ﴿14﴾
لَقَالُواْ إِنَّمَا سُكِّرَتْ أَبْصَٰرُنَا بَلْ نَحْنُ قَوْمٌ مَّسْحُورُونَ ﴿15﴾

Suratul Hijiri

A Makka Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Casa'in Da Tara (99)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabadaya, mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

Wannan sura ta ƙunshi Asahabul-hijiri da manaƙasha a cikin ƙudure-ƙuduren mushirikai da tabbatar da tashin alƙiyama da bayanin ikon Allah, da tunatar da mutum tashinsa na farko, da alaƙarsa da Malaikuda aljannu, da ƙissoshin ba'alin Annabawa Alaihimussalam, da hira tareda Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama'

(TAƘAITA BURI DA ZARGI KAN TSAWAITA SHI)

1.A.L.R. (Allah ne masani da abinda yake nufi da wannan,) Waɗannan ayoyi, ayoyi ne na littafi Alƙur'ani, ayoyin ƙur'anine mai bayyanawar ƙarya da gaskiya.

2. Da yawa kafirai zasu dinga burin dasun kasance Musulmai (ranar alƙiyama idan sun ga halinsu da halin Musulmai.)

3. Bar kafirai (Ya Annabi Muhammadu Sallallahu alaika wasallama) su ci suji daɗi, tsawaita buri da tsawon rai ya shagaltar dasu (ga buran imani,) da sannu zasu ga (ƙarshen al'amarınsu.)

4. Bamu halakar daga mutanen alƙaryaba face tana da littafi na ajali abin ambato (ga halakar da ita.)

5. Ba wata al'umma da take rigayar ajalinta, baza suyi jinkiri (ga buransa ba.)

6. Kafiran Makka suka faɗa wa (Annabi Sallallahu alaihi wasallama,) "Ya wanda aka saukar da alƙur'ani a gareshi,)a cikin riyawarsa,) haƙiƙa kai ba mai hankali ne ba.

7. "Donme bakazo mana da Mala'iku ba, in ka kasance daga magasgata (a cikin faɗin ka cewa kai Annabi ne, kuma wannan Alƙur'ani daga Allah yake?"

8. (Ubangiji yace,) "Mala'iku basa sauka saida gaskiya; azaba, basu kasance a yayin saukar Mala'ikuda azaba ababan saurarawa ba".

9. Haƙiƙa mune muka saukar da Alƙur'ani, haƙiƙa mu, masu kiyayewa ne a gareshi (daga canjawa da jirkitawa da daɗi da ragi.)

10. Haƙiƙa mun aiko gabanka jakadu a cikin mutanen farko, (jakadu ɗari ukuda goma sha uku,)

11. Wani manzo bazaizo musu face suna izgili dashi.

12. Hakana muke shigar da wannan ƙaryatawa a cikin zukatan masu laifi, (kafiran Makka da waninsu.)

13. Bazasu gasgatada Annabi (Sallallahu Alaihi wasallama) ba, haƙiƙa al'adar Allah a cikinsu ta shuɗe (na daga azabtar dasu saboda ƙaryata Annabawansu, to, waɗannan ma kamar su suke.)

14. Da mun ɓude ƙofa ta sama a garesu, suka zama suna hawa a cikinsa.

15. Dasunce, "Dahir dai an juyar da idanuwanmune kawai, kai! mu mutane ne ababan yiwa suddabaru".

وَلَقَدْ جَعَلْنَا فِي السَّمَاءِ بُرُوجًا وَزَيَّنَّاهَا لِلنَّاظِرِينَ ﴿16﴾
وَحَفِظْنَاهَا مِن كُلِّ شَيْطَانٍ رَّجِيمٍ ﴿17﴾ إِلَّا مَنِ اسْتَرَقَ
السَّمْعَ فَأَتْبَعَهُ شِهَابٌ مُّبِينٌ ﴿18﴾ وَالْأَرْضَ مَدَدْنَاهَا وَأَلْقَيْنَا
فِيهَا رَوَاسِيَ وَأَنبَتْنَا فِيهَا مِن كُلِّ شَيْءٍ مَّوْزُونٍ ﴿19﴾ وَجَعَلْنَا
لَكُمْ فِيهَا مَعَايِشَ وَمَن لَّسْتُمْ لَهُ بِرَازِقِينَ ﴿20﴾ وَإِن مِّن شَيْءٍ
إِلَّا عِندَنَا خَزَائِنُهُ وَمَا نُنَزِّلُهُ إِلَّا بِقَدَرٍ مَّعْلُومٍ ﴿21﴾
وَأَرْسَلْنَا الرِّيَاحَ لَوَاقِحَ فَأَنزَلْنَا مِنَ السَّمَاءِ مَاءً فَأَسْقَيْنَاكُمُوهُ
وَمَا أَنتُمْ لَهُ بِخَازِنِينَ ﴿22﴾ وَإِنَّا لَنَحْنُ نُحْيِي وَنُمِيتُ
وَنَحْنُ الْوَارِثُونَ ﴿23﴾ وَلَقَدْ عَلِمْنَا الْمُسْتَقْدِمِينَ مِنكُمْ
وَلَقَدْ عَلِمْنَا الْمُسْتَأْخِرِينَ ﴿24﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ هُوَ يَحْشُرُهُمْ إِنَّهُ حَكِيمٌ عَلِيمٌ ﴿25﴾
* وَلَقَدْ خَلَقْنَا الْإِنسَانَ مِن صَلْصَالٍ مِّنْ حَمَإٍ مَّسْنُونٍ ﴿26﴾ وَالْجَانَّ خَلَقْنَاهُ ثُمُن
مِن قَبْلُ مِن نَّارِ السَّمُومِ ﴿27﴾ وَإِذْ قَالَ رَبُّكَ لِلْمَلَائِكَةِ إِنِّي خَالِقٌ بَشَرًا
مِّن صَلْصَالٍ مِّنْ حَمَإٍ مَّسْنُونٍ ﴿28﴾ فَإِذَا سَوَّيْتُهُ وَنَفَخْتُ فِيهِ
مِن رُّوحِي فَقَعُوا لَهُ سَاجِدِينَ ﴿29﴾ فَسَجَدَ الْمَلَائِكَةُ كُلُّهُمْ
أَجْمَعُونَ ﴿30﴾ إِلَّا إِبْلِيسَ أَبَىٰ أَن يَكُونَ مَعَ السَّاجِدِينَ ﴿31﴾

(WANI ABU DAGA IKON ALLAH DA NI'IMOMINSA)

16. Haƙiƙa mun sanya burijai a cikin sama, (wato taurari goma sha biyu; hamalu, sauru, jauza'u, saraɗanu, asadu, sunbula, mizan, aƙarabu, ƙausu, jadyu, dalwu, da hutu. Waɗannan sune manzilolin taurari bakwai matafiya; murriha tana da hamalu da aƙarabu, zuhara tana da sauru da mizan, uɗaridu tana da jauza'u dasunbula, ƙamaru yana da saraɗanu, shamsu tana da asadu, mishtari yana da ƙausu da hutu, zuhal yana da jadyu da dalwu. Ubangiji yasanya amfani a cikin talikan ƙasa da waɗannan taurari kamar yadda ya sa amfani cikin ci da sha,) mun ƙawata tada taurari ga masu duba.
17. Mun kiyaye ta daga dukkan shaiɗanu ababan jifa.
18. Sai wanda ya sato ji, saitauraro mabayyani yabi shi (wato mashiyabi shiya ƙone shi ko ya huɗa shi.)
19. ƙasa mun shinfiɗa ta, mun kafa duwarwatsu matabbata a cikinta, mun tsiro da kowane abu aunanne a cikinta.
20. Mun sanya muku sabubban rayuwa a cikinta, mun sanya muku abinda baku kasance masu arzutuwa daga gareshi ba, (na daga bayi da dabbobi da bisashe, Allah ne yake azurta su.)
21. Babu daga wani abu face taskokinsa na garemu, Barna saukar dashi saida gwargwado abin sani (gwargwadon masalahar bayi, kuma gwargwadon nufin Allah da saninsa, ko ba masalahar bayi.)
22. Mun sako iskoki halin kasancewarsu masu barbarar girgije (saiya cika da ruwa) sai muka saukar da ruwa daga girgije, sai muka shayar daku ,shi, ku baku kasance masu taskacewa gareshi ba, (wato taskarsa bata wurinku.)
23. Haƙiƙa mune muke rayawa muke kashewa, mune kuma masu gadon (halitta.)
24. Haƙiƙa mun san magabata gareku (tun daga Annabi Adamu Alaihissalamu), haƙiƙa mun san majinkirta (izuwa ranar Alƙiyama.)
25. Haƙiƙa Ubangijinka shine yake tara su, haƙiƙa shi gwanine (cikin aikinsa) masanine (da halittarsa.)

(ƘISSAR ANNABI ADAMU ALAIHISSALAM DA HALITTARSA DA ALAƘARSA DA MALA'IKU)

26. Haƙiƙa mun halicci Annabi Adamu (Alaihissalam) daga yinɓu mai amo na daga baƙin taɓo mai ɗoyi.
27. Iblis kuma mun halicce shi tun gaban halittar Annabi Adamu (Alaihissalam) daga tacacciyar wuta mara hayaƙi take shiga cikin kafafan gashi.
28. Ka ambata zamanin da Ubangijinka ya faɗa ga Mala'iku, "Ni, haƙiƙa mai halittar mutumne daga kasko na taɓo mai ɗoyi.
29. "To idan na daidaita shi, na gudanar da raina a cikinsa, (ya zama mai rai,) to, ku faɗi kuna masu gaisuwa gareshi."
30. Sai Mala'iku sukayi sajada dukkan su bakiɗaya,
31. Sai Iblis (uban aljannu ya kasance tsakanin Mala'iku,) ya ƙiya kasance daga masuyin saj da.

قَالَ يَٰٓإِبۡلِيسُ مَا لَكَ أَلَّا تَكُونَ مَعَ ٱلسَّٰجِدِينَ ﴿32﴾ قَالَ لَمۡ
أَكُن لِّأَسۡجُدَ لِبَشَرٍ خَلَقۡتَهُۥ مِن صَلۡصَٰلٖ مِّنۡ حَمَإٖ مَّسۡنُونٖ ﴿33﴾
قَالَ فَٱخۡرُجۡ مِنۡهَا فَإِنَّكَ رَجِيمٞ ﴿34﴾ وَإِنَّ عَلَيۡكَ ٱللَّعۡنَةَ
إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلدِّينِ ﴿35﴾ قَالَ رَبِّ فَأَنظِرۡنِيٓ إِلَىٰ يَوۡمِ يُبۡعَثُونَ ﴿36﴾
قَالَ فَإِنَّكَ مِنَ ٱلۡمُنظَرِينَ ﴿37﴾ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡوَقۡتِ
ٱلۡمَعۡلُومِ ﴿38﴾ قَالَ رَبِّ بِمَآ أَغۡوَيۡتَنِي لَأُزَيِّنَنَّ لَهُمۡ
فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَأُغۡوِيَنَّهُمۡ أَجۡمَعِينَ ﴿39﴾ إِلَّا عِبَادَكَ مِنۡهُمُ
ٱلۡمُخۡلَصِينَ ﴿40﴾ قَالَ هَٰذَا صِرَٰطٌ عَلَيَّ مُسۡتَقِيمٌ ﴿41﴾ إِنَّ عِبَادِي
لَيۡسَ لَكَ عَلَيۡهِمۡ سُلۡطَٰنٌ إِلَّا مَنِ ٱتَّبَعَكَ مِنَ ٱلۡغَاوِينَ ﴿42﴾
وَإِنَّ جَهَنَّمَ لَمَوۡعِدُهُمۡ أَجۡمَعِينَ ﴿43﴾ لَهَا سَبۡعَةُ أَبۡوَٰبٖ لِّكُلِّ بَابٖ مِّنۡهُمۡ
جُزۡءٞ مَّقۡسُومٌ ﴿44﴾ إِنَّ ٱلۡمُتَّقِينَ فِي جَنَّٰتٖ وَعُيُونٍ ﴿45﴾ ٱدۡخُلُوهَا
بِسَلَٰمٍ ءَامِنِينَ ﴿46﴾ وَنَزَعۡنَا مَا فِي صُدُورِهِم مِّنۡ غِلٍّ إِخۡوَٰنًا عَلَىٰ
سُرُرٖ مُّتَقَٰبِلِينَ ﴿47﴾ لَا يَمَسُّهُمۡ فِيهَا نَصَبٞ وَمَا هُم مِّنۡهَا بِمُخۡرَجِينَ ﴿48﴾
۞ نَبِّئۡ عِبَادِيٓ أَنِّيٓ أَنَا ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿49﴾ وَأَنَّ عَذَابِي
هُوَ ٱلۡعَذَابُ ٱلۡأَلِيمُ ﴿50﴾ وَنَبِّئۡهُمۡ عَن ضَيۡفِ إِبۡرَٰهِيمَ ﴿51﴾

ربع

32. Ubangiji yace, "Ya kai Iblisu me ya hanaka ka kasance tareda masu sajada?"
33. Sai yace, Ban kasance zan yi sajada ba ga mutum daka halicce shi daga kasko na taɓo mai ɗoyi".
34. Sai yace, "Fita daga aljanna (ko daga sammai,) haƙiƙa kai abin kora ne.
35."Haƙiƙa tsinar albarka na kanka izuwa ranar sakamako".
36. Yace, "Ubangiji saurara min izuwa ranar tashin mutane,"
37. Yace, "Haƙiƙa kai kana cikin ababan saurarawa".
38. Izuwa ranar, Lokaci abin sani (wato busar farko".)
39. Yace, "Ubangiji saboda ɓatar dani daka yi, lalle zan ƙawata musu sabanni a cikin ƙasa, zan kuma halakar dasu bakiɗaya.

(RASHIN TASIRIN SHAIƊAN A KAN WALIYYAN ALLAH)

40. "Sai bayinka ababan tsarkakewa daga cikinsu".
41. Ubangiji yace, "Wannan tafarki ne madaidaici a garemu.
42. "Shine, haƙiƙa bayina muminai baka da karfi kansu, sai dai wanda yabika daga kafirai.
43. " Haƙiƙa jahannama lalle Itace ma'alkawartarsu bakiɗaya".
44. Tana da ruɓi bakwai, ga kowace kofa akwai yanki abin rabawa a garesu.
45. Haƙiƙa masu tsoron Allah suna cikin aljannatai da idanuwa na ruwa,
46. Ana cewa dasu, "Ku shige ta kuna makuɓuta daga dukkah abin tsoro kuna amintattu".
47. Mun fitar da abinda yake cikin ƙirazansu na daga ƙeta, halin kasancewarsu "yan uwa, suna kan gadaje suna kallon juna.
48. Wahala bazata samesu a cikinta ba, su baza a fitar dasu daga gareta ba har abada.
49. Baiwa bayina labari (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama,) haƙiƙa ni, nine mai yawan gafara (ga muminai) mai yawan jinƙai (dasu.)
50. Haƙiƙa azabata (ga masu saɓo) Itace azaba mai raɗaɗi.

(ƘISSAR BAKIN ANNABI IBRAHIM DA ANNABI LUƊU ALAIHIMUSSA-LAMU DA MUTANENSU)

51. Basu labari ga baƙin Annabi Ibrahima (tsiran Allah ya tabbata a gareshi, Mala'ikune guda goma sha biyu, Mala'ika Jibrilu Alaihissalam yana cikinsu.)

إِذْ دَخَلُوا۟ عَلَيْهِ فَقَالُوا۟ سَلَٰمًا قَالَ إِنَّا مِنكُمْ وَجِلُونَ ﴿52﴾ قَالُوا۟
لَا تَوْجَلْ إِنَّا نُبَشِّرُكَ بِغُلَٰمٍ عَلِيمٍ ﴿53﴾ قَالَ أَبَشَّرْتُمُونِي عَلَىٰٓ أَن
مَّسَّنِيَ ٱلْكِبَرُ فَبِمَ تُبَشِّرُونَ ﴿54﴾ قَالُوا۟ بَشَّرْنَٰكَ بِٱلْحَقِّ
فَلَا تَكُن مِّنَ ٱلْقَٰنِطِينَ ﴿55﴾ قَالَ وَمَن يَقْنَطُ مِن رَّحْمَةِ
رَبِّهِۦٓ إِلَّا ٱلضَّآلُّونَ ﴿56﴾ قَالَ فَمَا خَطْبُكُمْ أَيُّهَا ٱلْمُرْسَلُونَ ﴿57﴾
قَالُوٓا۟ إِنَّآ أُرْسِلْنَآ إِلَىٰ قَوْمٍ مُّجْرِمِينَ ﴿58﴾ إِلَّآ ءَالَ لُوطٍ إِنَّا
لَمُنَجُّوهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿59﴾ إِلَّا ٱمْرَأَتَهُۥ قَدَّرْنَآ إِنَّهَا لَمِنَ ٱلْغَٰبِرِينَ ﴿60﴾
فَلَمَّا جَآءَ ءَالَ لُوطٍ ٱلْمُرْسَلُونَ ﴿61﴾ قَالَ إِنَّكُمْ قَوْمٌ
مُّنكَرُونَ ﴿62﴾ قَالُوا۟ بَلْ جِئْنَٰكَ بِمَا كَانُوا۟ فِيهِ يَمْتَرُونَ ﴿63﴾
وَأَتَيْنَٰكَ بِٱلْحَقِّ وَإِنَّا لَصَٰدِقُونَ ﴿64﴾ فَاسْرِ بِأَهْلِكَ
بِقِطْعٍ مِّنَ ٱلَّيْلِ وَٱتَّبِعْ أَدْبَٰرَهُمْ وَلَا يَلْتَفِتْ مِنكُمْ أَحَدٌ
وَٱمْضُوا۟ حَيْثُ تُؤْمَرُونَ ﴿65﴾ وَقَضَيْنَآ إِلَيْهِ ذَٰلِكَ ٱلْأَمْرَ
أَنَّ دَابِرَ هَٰٓؤُلَآءِ مَقْطُوعٌ مُّصْبِحِينَ ﴿66﴾ وَجَآءَ أَهْلُ ٱلْمَدِينَةِ يَسْتَبْشِرُونَ ﴿67﴾
قَالَ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ ضَيْفِي فَلَا تَفْضَحُونِ ﴿68﴾ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ
وَلَا تُخْزُونِ ﴿69﴾ قَالُوٓا۟ أَوَلَمْ نَنْهَكَ عَنِ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿70﴾

52. Zamanin da suka shiga gareshi, sukace "Gaisuwa", yace, "Haƙiƙa mu masu tsoro ne daga gareku, (bayan ya bujirar musu abinci basu ci ba.)
53. Sukace, "Kada kaji tsoro, haƙiƙa mu, jakadun Ubangijinka ne, munayi maka albishir dayaro mai yawan ilimi (Ishaƙu".)
54. Yace, "Kwayi min albishir da ɗa a bisa tsufa daya cim min, da me kuke min albishir?" (wato neman tambayo ne na santi wato mana ki da farin ciki.)
55. Sukace, "Munyi maka albishir da gaskiya, kadaka kasance daga masu debe haso".
56. Yace, "Ba mai ɗebe haso daga rahamar Ubangijinsa sai ɓatattu".
57. Yace, "Meye sha'aninku, Yaku waɗannan jakadu?"
58. Sukace, " Haƙiƙa an aiko mune izuwa mutane masu laifi, (wato kafirai mutanen Annabi Luɗu Alaihissalam don mu halakar dasu")
59. Sai iyalin Annabi Luɗu (Alaihissalam,) haƙiƙa mu, zamu tserar dasu bakiɗya (saboda imaninsu.)
60. "Sai mata tasa mun kaddara cewa tasa, haƙiƙa ita, tana daga masu wanzuwa (a cikin azaba saboda kafircinta".)
61. Yayin dajakadu suka zowa Annabi Luɗu (Alaihissalam,)
62. Sai yace (dasu,) " Haƙiƙa ku mutane ne ababan musu, (wato ban san ku ba".)
63. Sukace, " Haƙiƙa mun zo maka da abinda suka kasance suna kokonto dashi (shine azaba.)
64. "Mun zo maka da gaskiya, haƙiƙa mu magasgata ne (a cikin maganannu.)
65. "Sai ka tafi da iyalinka dayankin dare ka bi bayansu, ka da wani ɗaya yayi waiwaye daga cikinku, (don kada ya ga abindazai saiikar musu na azaba,) ku wuce inda aka umarce ku (Sham, Allah ya naɗe musu ƙasa a lokacin suka tsira suka sadu da Annabi Ibrahim alaihissalam, tafiyar farsahi hudu ce tsakaninsu.)
66. Muka aiko da wannan al'amari izuwa gareshi, shine haƙiƙa asalin waɗannan mutane abin yankewa ne da asuba.
67. Mutanen wannan gari sukazo suna muma, (wato birnin Sazuma don an gaya musu cewa akwai baƙin samari kyawawa a gi-dan Annabi Luɗu Alaihissalam, su kuwa Mala'iku ne.)
68. Annabi Luɗu Alaihissalam yace, "Waɗannan baƙina ne, ka daku ,kunyata ni.
69. "Kuji tsoron Allah kadaku ,kunyata ni (da nufin ɓarna dasu".)
70. Sukace, "Bamu hane ka ga buran saukar ɓaki ba ne?".

قَالَ هَٰٓؤُلَآءِ بَنَاتِيٓ إِن كُنتُمۡ فَٰعِلِينَ ﴿٧١﴾ لَعَمۡرُكَ إِنَّهُمۡ لَفِي
سَكۡرَتِهِمۡ يَعۡمَهُونَ ﴿٧٢﴾ فَأَخَذَتۡهُمُ ٱلصَّيۡحَةُ مُشۡرِقِينَ ﴿٧٣﴾
فَجَعَلۡنَا عَٰلِيَهَا سَافِلَهَا وَأَمۡطَرۡنَا عَلَيۡهِمۡ حِجَارَةٗ مِّن سِجِّيلٍ ﴿٧٤﴾
إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّلۡمُتَوَسِّمِينَ ﴿٧٥﴾ وَإِنَّهَا لَبِسَبِيلٖ مُّقِيمٍ ﴿٧٦﴾
إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ لِّلۡمُؤۡمِنِينَ ﴿٧٧﴾ وَإِن كَانَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡأَيۡكَةِ
لَظَٰلِمِينَ ﴿٧٨﴾ فَٱنتَقَمۡنَا مِنۡهُمۡ وَإِنَّهُمَا لَبِإِمَامٖ مُّبِينٖ ﴿٧٩﴾
* وَلَقَدۡ كَذَّبَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡحِجۡرِ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ﴿٨٠﴾ وَءَاتَيۡنَٰهُمۡ ءَايَٰتِنَا فَكَانُواْ ثمن
عَنۡهَا مُعۡرِضِينَ ﴿٨١﴾ وَكَانُواْ يَنۡحِتُونَ مِنَ ٱلۡجِبَالِ بُيُوتًا ءَامِنِينَ ﴿٨٢﴾
فَأَخَذَتۡهُمُ ٱلصَّيۡحَةُ مُصۡبِحِينَ ﴿٨٣﴾ فَمَآ أَغۡنَىٰ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ
يَكۡسِبُونَ ﴿٨٤﴾ وَمَا خَلَقۡنَا ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَآ إِلَّا بِٱلۡحَقِّۗ
وَإِنَّ ٱلسَّاعَةَ لَأٓتِيَةٞۖ فَٱصۡفَحِ ٱلصَّفۡحَ ٱلۡجَمِيلَ ﴿٨٥﴾ إِنَّ رَبَّكَ
هُوَ ٱلۡخَلَّٰقُ ٱلۡعَلِيمُ ﴿٨٦﴾ وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَٰكَ سَبۡعٗا مِّنَ ٱلۡمَثَانِي وَٱلۡقُرۡءَانَ
ٱلۡعَظِيمَ ﴿٨٧﴾ لَا تَمُدَّنَّ عَيۡنَيۡكَ إِلَىٰ مَا مَتَّعۡنَا بِهِۦٓ أَزۡوَٰجٗا مِّنۡهُمۡ
وَلَا تَحۡزَنۡ عَلَيۡهِمۡ وَٱخۡفِضۡ جَنَاحَكَ لِلۡمُؤۡمِنِينَ ﴿٨٨﴾ وَقُلۡ إِنِّيٓ
أَنَا ٱلنَّذِيرُ ٱلۡمُبِينُ ﴿٨٩﴾ كَمَآ أَنزَلۡنَا عَلَى ٱلۡمُقۡتَسِمِينَ ﴿٩٠﴾

71. Yace, "Wadannan"ya"'yana ne mata, in kun kasance masu aikata (abinda kuke so na sha'awa, to, ku aure su".)
72. Ubangiji yace; "Na rantse da rayuwarka, haƙiƙa su suna diriricewa a cikin magaginsu".
73. Tsawar (Mala'ika Jibrilu Alaihissalam) ta kama su, azamanin asuba,
74. Muka sanya saman ƙasan alkaryinsu kasanta, (shine Mala'ika Jibrilu Alaihissalam, ya ɗaga ta izuwa sama, ya juyo da ita a kife izuwa ƙasa») muka saki ruwan duwarwatsu a kansu na daga ƙonannan yunbu.
75. Haƙiƙa akwai ayoyi a cikin wancananka (na kaɗaitar Allah,) ga masu duba don izna.
76. Haƙiƙa alƙaryatun Annabi Luɗu (Alaihissalam) suna taƙarki matabbaci, (tafarkin ƙuraishu zuwa Sham bata ɓata ba.)
77. Haƙiƙa akwai izna a cikin wancananka ga muminai.

(ƘISSAR MUTANEN RUNƘUNƘA DA HIJIRU)

78. Haƙiƙa ma'abota Runƙunƙa sun kasance azzalumai (kusa da madayana take, sune mutanen Annabi Sha'aibu Alaihissalam) sun zalunci kansu da ƙaryata shi.
79. Mukayi azabadaga garesu, Allah ya ƙone su da mnfar wuta, amma mutanen madayana an halakar dasu da tsawa, wato an aiko shi izuwa mutane biyu wato mutanen Runƙuƙa da Laika wato Madayana. To, haƙiƙa su (alƙaryun Annabi Luɗu Alaihissalam da Runkunƙa) suna a hanya mabayyaniya.
80. Haƙiƙa mutanen Hijiru sun ƙaryata manzanni (zaza ne tsakanin Madina da Sham, sune Samudawa saboda sun ƙaryata Annabi Salihu ALaihissalam, ya zama kamar sun ƙaryata sauran manzannin ke nan saboda sunyi tarayya a cikin zuwa da tauhidi.)
81. Mun basu ayoyinmu (taguwa) suka kasance masu bujirewa ga buranta.
82. Sun kasance suna sassaƙa ɗakuna daga duwarwatsu suna amintattu.
83. Tsawa ta kama su da asuba.
84. Abinda suke aikatawa (na ginegine da tara dukiya) bai wadatar dasu komai (daga azabar Allah ba,)
85. Bamu halicci sammai da ƙassaida abinda yake cikinsu ba, saida gaskiya, haƙiƙa alƙiyama mai zuwa ce, kayi rangwame, rangwame kyakkyawa.
86. Haƙiƙa Ubangijinka shine mahalicci da komai masani da komai.

(GANAWAR UBANGIJI TAREDA MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

87. Haƙiƙa mun baka bakwai na ababan biyantawa, (Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama yace "Itace Fatiha, saboda ana maimaita ta a kowace raka'a",) mun baka alƙur'ani maigirma.
88. Kadaka mika idanuwanka izuwa abinda muka jiyar da nau'o'insu daɗi dashi, kada kayi baƙin ciki a kansu (in basu bada gaskiya ba,) ka ƙaskantar da fuffukenka, (wato kayi tawali'u) ga muminai.
89. Cene, " Haƙiƙa ni, mai gargaɗi ne da azabar Allah (kadata sauka a gareku,) mabayyanin gargaɗi.
90. Tamfar yadda muka saukar da azaba ga masu rarrabawa (tsakanin littattafai ababan saukarwa sune Yahudu da Nasara.)

ٱلَّذِينَ جَعَلُواْ ٱلْقُرْءَانَ عِضِينَ ﴿91﴾ فَوَرَبِّكَ لَنَسْـَٔلَنَّهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿92﴾
عَمَّا كَانُواْ يَعْمَلُونَ ﴿93﴾ فَاصْدَعْ بِمَا تُؤْمَرُ وَأَعْرِضْ
عَنِ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿94﴾ إِنَّا كَفَيْنَـٰكَ ٱلْمُسْتَهْزِءِينَ ﴿95﴾ ٱلَّذِينَ يَجْعَلُونَ
مَعَ ٱللَّهِ إِلَـٰهًا ءَاخَرَ فَسَوْفَ يَعْلَمُونَ ﴿96﴾ وَلَقَدْ نَعْلَمُ
أَنَّكَ يَضِيقُ صَدْرُكَ بِمَا يَقُولُونَ ﴿97﴾ فَسَبِّحْ بِحَمْدِ رَبِّكَ
وَكُن مِّنَ ٱلسَّـٰجِدِينَ ﴿98﴾ وَاعْبُدْ رَبَّكَ حَتَّىٰ يَأْتِيَكَ ٱلْيَقِينُ ﴿99﴾

16 سُورَةُ النَّحْلِ مَكِّيَّةٌ

وَآيَاتُهَا ثَمَانٍ وَعِشْرُونَ وَمِائَةٌ 128

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَـٰنِ ٱلرَّحِيمِ

* أَتَىٰٓ أَمْرُ ٱللَّهِ فَلَا تَسْتَعْجِلُوهُ سُبْحَـٰنَهُۥ وَتَعَـٰلَىٰ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿1﴾ ربع
يُنَزِّلُ ٱلْمَلَـٰٓئِكَةَ بِٱلرُّوحِ مِنْ أَمْرِهِۦ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦٓ
أَنْ أَنذِرُوٓاْ أَنَّهُۥ لَآ إِلَـٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَاتَّقُونِ ﴿2﴾ خَلَقَ ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ
بِٱلْحَقِّ تَعَـٰلَىٰ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿3﴾ خَلَقَ ٱلْإِنسَـٰنَ مِن نُّطْفَةٍ فَإِذَا
هُوَ خَصِيمٌ مُّبِينٌ ﴿4﴾ وَٱلْأَنْعَـٰمَ خَلَقَهَا لَكُمْ فِيهَا دِفْءٌ وَمَنَـٰفِعُ وَمِنْهَا
تَأْكُلُونَ ﴿5﴾ وَلَكُمْ فِيهَا جَمَالٌ حِينَ تُرِيحُونَ وَحِينَ تَسْرَحُونَ ﴿6﴾

91. Wađanda suka mayar da littattafansu da aka saukar abar rarrabawa suka bada gaskiya da sashi suka kafirce da sashi.
92. Na rantse da Ubangijinka zamu tambaye su bakiđaya,
93. Ga abinda suka kasance suna aikatawa.
94. Bayyana ƙarara da abinda aka umarce ka, ka bujire ga buran mushirikai.
95. Haƙiƙa mu, mun isar maka masu izgili dan kai, (sune Walidu đan Mugira da Asi dan Wa'ilu da Adiyu đan ƙaisu da Aswadu dan Abdul muđđalibu -da Aswadu đan Abdul -yagusa.)
96. Wađanda suka sanya wani Ubangiji daban tareda Allah, to, da sannu zasu san ƙarshen al'amarinsu.)

(DUKKAN TSAWON RANKA BAI SHIGE AWA DAYA BA, SANYASHI CIKIN DA'AR UBANGIJI.)

97. Haƙiƙa mun san lalle ƙirjinka yana ƙuntata saboda abinda suke fađa (na izgili da ƙaryatawa.)
98. To, sai kayi tasbihi da godiyar Ubangijinka, (Cene, "Subuha-nallahiwa-bihamdihi") ka kasance cikin masu sajada (wato masallata.)
99. Bautawa Ubangijuika hai mutuwa tazo maka.

Suratul Nahali

A Makka Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Dari Da Ishirin DaTakwas (128)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a dauniyagabađaya, mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

Ana ambaton ta Suratun Ni'ami saboda abinda Allah ya kirga a cikinta na daga ni'imomi, da bayanin mabayyanar ikon Allah. Ta ƙunshi munaƙasha da mushirikai a cikin ƙudure-ƙudurensu, da zance cikin ranar alƙiyama, ƙarshen surar kuma yayi magana kan masu izgili da ambaton mutuwa)

(TABBATAR DA ZUWAN ALƘIYAMA)

1. Alƙiyama ta zo, (wato zata zo, an fađi haka don tabbatar da zuwanta,) kadaku ,neme shi gaban lokacinsa. Tsarki ya tabbatarwa Ubangiji, Ya girma ga dukkan abinda kuke shirkantawa dashi. (IKON ALLAH)
2. Yana saukar da Mala'ika Jibrilu (Alaihissalam) da wahayi da nufinsa a bisa wanda yaga dama daga bayinsa, (sune Annabawa Alaihimussalam,) cewa ku tsoratar da kafirai da azabar Allah, ku sanar dasu cewe lallai babu abin bautawa da gaskiya sai ni, tokujitsprona.
3. Ya halicci sammai da ƙassaida gaskiyaya girma ga buran abinda suke shirkantawa dashi, (na gumaka.)
4. Ya halicci mutum daga maniyyi har ya maidashi ƙaƙƙarfa, sai gashi mai tsananin husuma mabayyaninta (a cikin kore tashin alƙiyama, yana cewa wayake raya ƙasusuwa alhali tana rididdigaggiya?)
5. Yahalicci dabbobi (rakuma da shanu da tumakai) kuma da jin đimi a cikinta (na daga tufafi da mayafai daga gasunta, da audigar gashinta, wato sufinta kuma da anfanuuwa na daga "ya"yanta bubbugar nonontada hawanta,) kuna ci daga gareta.
6. Ado na gareku a cikinta lokacin da kuke maida ita izuwa makwancinta, da lokacin da kuke fitar da ita izuwa makiyaya da safe.

وَتَحۡمِلُ أَثۡقَالَكُمۡ إِلَىٰ بَلَدٍ لَّمۡ تَكُونُواْ بَٰلِغِيهِ إِلَّا بِشِقِّ
ٱلۡأَنفُسِۚ إِنَّ رَبَّكُمۡ لَرَءُوفٞ رَّحِيمٞ 7 وَٱلۡخَيۡلَ وَٱلۡبِغَالَ
وَٱلۡحَمِيرَ لِتَرۡكَبُوهَا وَزِينَةٗۚ وَيَخۡلُقُ مَا لَا تَعۡلَمُونَ 8
وَعَلَى ٱللَّهِ قَصۡدُ ٱلسَّبِيلِ وَمِنۡهَا جَآئِرٞۚ وَلَوۡ شَآءَ
لَهَدَىٰكُمۡ أَجۡمَعِينَ 9 هُوَ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗۖ
لَّكُم مِّنۡهُ شَرَابٞ وَمِنۡهُ شَجَرٞ فِيهِ تُسِيمُونَ 10 يُنۢبِتُ
لَكُم بِهِ ٱلزَّرۡعَ وَٱلزَّيۡتُونَ وَٱلنَّخِيلَ وَٱلۡأَعۡنَٰبَ وَمِن
كُلِّ ٱلثَّمَرَٰتِۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ لِّقَوۡمٖ يَتَفَكَّرُونَ 11
وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ وَٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَۖ
وَٱلنُّجُومُ مُسَخَّرَٰتُۢ بِأَمۡرِهِۦٓۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ
يَعۡقِلُونَ 12 وَمَا ذَرَأَ لَكُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ مُخۡتَلِفًا أَلۡوَٰنُهُۥٓۚ
إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ لِّقَوۡمٖ يَذَّكَّرُونَ 13 وَهُوَ ٱلَّذِي
سَخَّرَ ٱلۡبَحۡرَ لِتَأۡكُلُواْ مِنۡهُ لَحۡمٗا طَرِيّٗا وَتَسۡتَخۡرِجُواْ مِنۡهُ
حِلۡيَةٗ تَلۡبَسُونَهَاۖ وَتَرَى ٱلۡفُلۡكَ مَوَاخِرَ فِيهِ
وَلِتَبۡتَغُواْ مِن فَضۡلِهِۦ وَلَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ 14

7. Tana ɗaukar nauyaye nauyayen ku izuwa gari da baku kasance masu isarsa ba saida wahala (kamar) Makka ko waninta,) haƙiƙa Ubangijinku mai tsananin jinƙai ne da rahama daku ,(daya halicce ta don ku.)

ƘAGE - ƘAGENCI GABAN ZAMANI

8. Ya halicci dawakai da alfadarai da jakai don ku hauta (kuma kuyı ado da hawanta, yana halittar abinda baku sani ba (na daga al'amura masu ban mana ki kamar mota, babur, jirgin ruwa, jirgin ƙasa, basukur, jirgin sama, radiyo da talbijin da tarho da kwamfiyutada sauran irinsu.)
9. Bayanin hanya madaidaiciya na ga Allah, akwai daga gareta tafarki karkatacce, dayaga damar shiryar ku (daya shirye ku izuwa madaidaicıyar nan) baki ɗaya.

(YANA DAGA NFIMOMINSA HAR YAU)

10. Shine wanda ya saukar da ruwa daga sama, abin sha na gareku daga gareshi da kuke shan sa, da itaciya da kuke kiwatar da dabbobin ku acikinta.
11. Yana tsuro mukuda hatsi dashi da zaitun da dabinai da inabai kuma daga dukkan "ya"yan itatuwa, akwai aya (mai shiryarwa bisa kaɗaitakar Allah) a cikin wancananka ga mutane dasuke tunani (a cikin aikin Allah.)
12. Ya hore muku dare da wuni da rana, da watada taurari ababan horewa da nufin Allah, akwai ayoyi cikin wancananka ga mutane masu hankali.
13. Ya hore muku abinda ya halitta a cikin ƙasa don ku (na daga mai rai da tsiri da wanin wannan) wanda kamanninsa suka sassaɓa ƙkamar ja dayar'ani da kore da waninsa,) haƙiƙa akwai aya a cikin wancananka ga mutane masu wa'azantuwa.
14. Shine wanda ya hore muku kogi ku hau shi kuyi nutso a cikinsa, dan Kuci nama ɗanye daga gareshi, (shine kifi) ku fito da kayan ado da kuke ɗaura ta daga cikinsa (shine lu'u'lu'u da murjan,) kana ganin jiraga masu keta ruwa a cikinsa suna kaiwa da komowa, da iska guda ɗaya (ko ƙarfin inji) kuma don ku nema daga falalarsa (ta wajen ciniki ko neman lada da zuwa hajji ko ziyarar Annabawa da Waliyyai da neman ilimi) don ku godewa Ubangiji a kan wannan.

ثمن

* وَأَلْقَىٰ فِي الْأَرْضِ رَوَاسِيَ أَن تَمِيدَ بِكُمْ وَأَنْهَٰراً وَسُبُلاً
لَّعَلَّكُمْ تَهْتَدُونَ ﴿15﴾ وَعَلَٰمَٰتٍ وَبِالنَّجْمِ هُمْ يَهْتَدُونَ ﴿16﴾
أَفَمَن يَخْلُقُ كَمَن لَّا يَخْلُقُ أَفَلَا تَذَّكَّرُونَ ﴿17﴾
وَإِن تَعُدُّواْ نِعْمَةَ اللَّهِ لَا تُحْصُوهَا إِنَّ اللَّهَ لَغَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿18﴾
وَاللَّهُ يَعْلَمُ مَا تُسِرُّونَ وَمَا تُعْلِنُونَ ﴿19﴾ وَالَّذِينَ
تَدْعُونَ مِن دُونِ اللَّهِ لَا يَخْلُقُونَ شَيْئاً وَهُمْ يُخْلَقُونَ ﴿20﴾
أَمْوَاتٌ غَيْرُ أَحْيَاءٍ وَمَا يَشْعُرُونَ أَيَّانَ يُبْعَثُونَ ﴿21﴾
إِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَاحِدٌ فَالَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِالْآخِرَةِ قُلُوبُهُم
مُّنكِرَةٌ وَهُم مُّسْتَكْبِرُونَ ﴿22﴾ لَا جَرَمَ أَنَّ اللَّهَ يَعْلَمُ مَا يُسِرُّونَ
وَمَا يُعْلِنُونَ إِنَّهُ لَا يُحِبُّ الْمُسْتَكْبِرِينَ ﴿23﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُم
مَّاذَا أَنزَلَ رَبُّكُمْ قَالُواْ أَسَاطِيرُ الْأَوَّلِينَ ﴿24﴾ لِيَحْمِلُواْ أَوْزَارَهُمْ
كَامِلَةً يَوْمَ الْقِيَٰمَةِ وَمِنْ أَوْزَارِ الَّذِينَ يُضِلُّونَهُم بِغَيْرِ عِلْمٍ
أَلَا سَاءَ مَا يَزِرُونَ ﴿25﴾ قَدْ مَكَرَ الَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ
فَأَتَى اللَّهُ بُنْيَٰنَهُم مِّنَ الْقَوَاعِدِ فَخَرَّ عَلَيْهِمُ السَّقْفُ
مِن فَوْقِهِمْ وَأَتَىٰهُمُ الْعَذَابُ مِنْ حَيْثُ لَا يَشْعُرُونَ ﴿26﴾

15. Ya kafa duwarwatsu tabbatattu a cikin ƙasa don kar tayi motsi da ku, yasanya ƙoramu da hanyoyi a cikinta don ku shirya izuwa manufarku
16. Ya halicci alamomi da kuke kafa dalili da ita (a kan hanyoyi kamar duwarwatsu da rana,) su suna shirya da taurari (izuwa hanyoyi da alƙibla [1] da sanin lokatai) hakana alƙibla wacce malamai suke fid da ita wacce suke ambatanta alƙibla, da agogo ta hannu ko ta aljihu ko ta kan tebur.)

(WANNAN SHINE MAHALICCI MAI JIBINTA NPIMA, INA GUMAKA?)

17. Yanzu wanda yake halitta (shine Allah,) zaizama kamar wanda baya halitta (shine gumaka) (A'A), lokacin da kuke shirkantawa dashi a cikin bauta) Shin ba kwa wa'azantuwa?
18. In kun ƙirga ni'imar Ubangiji bazaku iya kewayewa da ita ba, (ballantana ku iya samun gode mata,) haƙiƙa Ubangiji mai gafara ne mai jinƙai, (lokacin da yake muku ni'ima tareda saɓonsa da kuke yi.)
19. Allah yasan abinda kuke bayyanawa da abinda kuke ɓoyewa.
20. Waɗanda kuke bautawa ba Allah ba (sune gumaka) basa halittar komai, su ake halitta, (ake halittar su daga duwarwatsu ko waninta.)
21. Matattu ne (ba rai a cikinsu,) ba rayayyu ba ne, basu san lokacin daza a tashe su ba, (ƙaƙa za a bauta musu, don ba a bautawa kowa sai Ubangiji rayayye masanin asirin ɓoye.)
22. Ubangijinku, Ubangiji ne guda ɗaya, (ba kini gareshi a sifofinsa ko zatinsa, shine Allah,) waɗanda basu bada gaskiya da ranar Lahira ba, zukatansu masu musun (kaɗaitakar Allah ne,) su masu girman kaine (ga buran bada gaskiya da ita.)
23. Lallai haƙiƙa Ubangiji yasan abinda suke ɓoyewa da bayyanawa (zaiyi musu sakamako da wannan,) haƙiƙa Ubangiji ba yason masu girman kai.

(MASU GIRMAN KAI DA SAKAMAKONSU)

24. Idan Ance dasu me Ubangijinku ya saukar (a bisa Annabi Sallallahu alaihi wasallama) saisu ce, "Karyace-karyacen mutanen farko ne (don ɓatar da mutane".)
25. Sun faɗi haka don a ƙarshen al'amarin su ɗauki zunubansu cikakkiya (ba a kankare komai daga gareta ba) ranar alƙiyama, su dauka kuma daga sashin zunuban waɗanda suke ɓashshe su bada ilimi ba don (sun kira su izuwa bata sukabi su sukayi tarayya a cikin zunubi,) to, jama'a abinda suke ɗauka ɗinnan ya mugusta.
26. Haƙiƙa waɗanda suke gabansu sun yi makirci (shine Numruzu ya gina bene mai tsawo a Babila donya hau daga gareshi izuwa sama ya yaƙi mutanenta, Ubangiji yanufi ginin nan nasu daga harsashinsa ya aiko musu iska da girgizar ƙasa ta rushe, rufin benan ya fado a kansu, daga birbishin su su suna ƙarƙashinsa) azabatazo musu ta inda basuyi hasashe ba.

(1) Ya kamata ga dukkan musulmi ya lazumci wannan ala ta alƙibla inda duk yake, saboda bai san inda salla zata kama shi ba, a lazumce-ta kamar yadda ake lazumtar agogo. - Sanajiy -

ثُمَّ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ يُخۡزِيهِمۡ وَيَقُولُ أَيۡنَ شُرَكَآءِيَ ٱلَّذِينَ
كُنتُمۡ تُشَٰٓقُّونَ فِيهِمۡۚ قَالَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَ إِنَّ
ٱلۡخِزۡيَ ٱلۡيَوۡمَ وَٱلسُّوٓءَ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ ﴿27﴾ ٱلَّذِينَ تَتَوَفَّىٰهُمُ
ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ ظَالِمِيٓ أَنفُسِهِمۡۖ فَأَلۡقَوُاْ ٱلسَّلَمَ مَا كُنَّا نَعۡمَلُ مِن سُوٓءِۭۚ
بَلَىٰٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمُۢ بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ﴿28﴾
فَٱدۡخُلُوٓاْ أَبۡوَٰبَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَاۖ فَلَبِئۡسَ مَثۡوَى ٱلۡمُتَكَبِّرِينَ ﴿29﴾
* وَقِيلَ لِلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ مَاذَآ أَنزَلَ رَبُّكُمۡۚ قَالُواْ خَيۡرٗاۗ
لِّلَّذِينَ أَحۡسَنُواْ فِي هَٰذِهِ ٱلدُّنۡيَا حَسَنَةٞۚ وَلَدَارُ ٱلۡأٓخِرَةِ خَيۡرٞۚ
وَلَنِعۡمَ دَارُ ٱلۡمُتَّقِينَ ﴿30﴾ جَنَّٰتُ عَدۡنٖ يَدۡخُلُونَهَا
تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ لَهُمۡ فِيهَا مَا يَشَآءُونَۚ
كَذَٰلِكَ يَجۡزِي ٱللَّهُ ٱلۡمُتَّقِينَ ﴿31﴾ ٱلَّذِينَ تَتَوَفَّىٰهُمُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ طَيِّبِينَ
يَقُولُونَ سَلَٰمٌ عَلَيۡكُمُ ٱدۡخُلُواْ ٱلۡجَنَّةَ بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ﴿32﴾
هَلۡ يَنظُرُونَ إِلَّآ أَن تَأۡتِيَهُمُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ أَوۡ يَأۡتِيَ أَمۡرُ
رَبِّكَۚ كَذَٰلِكَ فَعَلَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ
وَمَا ظَلَمَهُمُ ٱللَّهُ وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ﴿33﴾

ربع

27. Sannan ranar alƙiyama zai kunyatar dasu yace (dasu bisa harshen Mala'iku don muzantawa garesu,) "Ina ababan tarayyar nawa (da kuke riyawa) wanda kuka kasance kuna sabawa (muminai a cikin lamarinsu,) waƙanda aka basu ilimi (sune Annabawa da muminai) suna cewa " Haƙiƙa kunyata a yau da mummunar makoma ta tabbata ga kafirai, (zasu faɗa musu haka ne don ganganko garesu.)

28. Waɗanda Mala'iku suke karɓar ransu suna zaluntar kansu (da kafirci,) to, sun jawu yayin mutuwa suna masu cewa bamu ka-sance muna aikata wani abu mummuna ba (wato shirka,) sai Mala'iku su ce (dasu kubar wannan magana kun yi mummuna.) " Haƙiƙa Ubangiji masanine da abinda kuka kasance kuna aikatawa.

29. "To, ku shiga kofofin jahannama, masu dauwama a cikinta, kai tur da makomar masu girman kai".

(MASU TSORON ALLAH DA SAKAMAKONSU)

30. Aka faɗa ga waɗanda suke jin tsoron Allah, "Me Ubangijinku ya saukar", sai Sukace, "Ya saukar da alheri". Rayuwa kyakkyawa ta tabbata ga waɗanda sukayi kyakkyawan aiki (a cikin wannan duniya, gidan lahira shine yafi (daga duniya da abinda yake cikinta,) madalla gidan masu tsoron Allah ita!

31. Aljannatai na dauwama suna shigarta, koramu suna gudana ƙarƙashinta abinda suke buƙata na garesu a cikinta, kamar irin wannan sakamako muke sakawa masu tsoron Allah.

32. (Su ne) waɗanda Mala'iku suke karɓar ransu suna tsarkaka (daga kafirci) suna ce dasu (yayin mutuwa,) "Gaisuwa ta tabbata garcku (a lahira" kuma ana ce dasu) "Ku shiga aljanna saboda abinda kuka kasance kuna aikatawa".

(KARSHEN KAFIRAI)

33. (Su kafirai) basa sauraron komai sai Mala'iku su zo su karɓi rayukansu, ko al'amarin Ubangijinka yazo, (azabako alƙiyama) kamar da waɗannan suka aikata hakana waɗanda suke gabansu suka aikata (na daga al'ummai waɗanda suka ƙaryata manzanninsu aka halakar dasu,) Allah bai zalunce su (da halakar dasu ba.da zunubi,) sai dai sun kasance kansu kaɗai suke zalunta (da kafirci.)

فَأَصَابَهُمْ سَيِّـَٔاتُ مَا عَمِلُواْ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿34﴾
وَقَالَ ٱلَّذِينَ أَشْرَكُواْ لَوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَا عَبَدْنَا
مِن دُونِهِۦ مِن شَيْءٍ نَّحْنُ وَلَآ ءَابَآؤُنَا وَلَا حَرَّمْنَا
مِن دُونِهِۦ مِن شَيْءٍ كَذَٰلِكَ فَعَلَ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ
فَهَلْ عَلَى ٱلرُّسُلِ إِلَّا ٱلْبَلَٰغُ ٱلْمُبِينُ ﴿35﴾ وَلَقَدْ بَعَثْنَا
فِي كُلِّ أُمَّةٍ رَّسُولًا أَنِ ٱعْبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱجْتَنِبُواْ ٱلطَّٰغُوتَ
فَمِنْهُم مَّنْ هَدَى ٱللَّهُ وَمِنْهُم مَّنْ حَقَّتْ عَلَيْهِ ٱلضَّلَٰلَةُ
فَسِيرُواْ فِي ٱلْأَرْضِ فَٱنظُرُواْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلْمُكَذِّبِينَ ﴿36﴾
إِن تَحْرِصْ عَلَىٰ هُدَىٰهُمْ فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِي مَن يُضِلُّ
وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ﴿37﴾ ۞ وَأَقْسَمُواْ بِٱللَّهِ جَهْدَ أَيْمَٰنِهِمْ ثمن
لَا يَبْعَثُ ٱللَّهُ مَن يَمُوتُ بَلَىٰ وَعْدًا عَلَيْهِ حَقًّا
وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿38﴾ لِيُبَيِّنَ لَهُمُ
ٱلَّذِي يَخْتَلِفُونَ فِيهِ وَلِيَعْلَمَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ
أَنَّهُمْ كَانُواْ كَٰذِبِينَ ﴿39﴾ إِنَّمَا قَوْلُنَا لِشَيْءٍ
إِذَآ أَرَدْنَٰهُ أَن نَّقُولَ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ﴿40﴾

34. Sakamakon abinda suka aikata ya same su, abinda suka kasance suna izgili dashi (na azaba) ya sauka garesu.
35. Wađanda sukayi shirka (na mutanen Makka Sukace, "Da Allah yaga dama bazamu bautawa wani abu, bashi ba, mu wala iyayenmu bazamu haramta wani abu ba koma bayansa, (na daga nonon gunki da bayan gunki da waninsu, to, shirkarmu da haramtawarmu da nufinsa ne, to, ashe shiya yarda dashi ke nan". Ubangiji yace,) "Hakana wađanda suke gabansu suka aikata (suka ƙaryata manzanninsu cikin abinda sukazo musu dashi,) to, ba wani abu a kan manzanni sai ida sako mabayyani (shiryarwa na ga Allah.)
36. Haƙiƙa mun aiko manzo a cikin dukkan al'umma tamfar da muka aiko ka a cikin wađannan, cewa ku bautawa Allah ku kađaita shi ku nisanci gumaka (kar ku bauta mata,) to, akwai daga garesu wanda Allah ya shirye shi (ya bada gaskiya) akwai daga garesu wanda ɓata ya wajaba gareshi (a cikin sanin Allah bai bada gaskiya ba,) to, kuyi tafiya (ku kafiran Makka) a cikin ƙasa, yaya ƙarshen wađanda suka ƙaryata manzanninsu ya kasance? (Sun halaka.)
37. In kai kwađayi (Ya Muhammadu Sallallahu alaika wasallama) bisa shiriyar dasu (alhali Ubangiji ya halakar dasu,) bazaka sami iko kan wannan ba, to, haƙiƙa Ubangiji baya shiryar da wanda ya ɓatar, basu da masu hana musu azabar Allah.
38. Sun rantse da Allah iyakacin rantsuwarsu Allah bazai tashi wanda ya mutu ba, (Allah yace,) kai tashin su zai yi, ya alƙawarta wannan a kansa alƙawartawa ya tabbatar dashi tabbatarwa, sai dai mafi yawan mutane basu san haka ba.
39. Zai tashe su donya bayyana musu abinda suke saɓani da muminai acikin sa (tareda muminai na al'amarin addini, yayi musu azabaya sakawa muminai da aljanna) kuma don wađanda suka kafirta su san haƙiƙa sun kasance m'aƙaryata (a cikin musun tashin alƙiyama.)
40. Dahir dai, fađinmu ga abu idan muka nufi samar dashi mu ce dashiya samu, to, shi saiya samu.

وَالَّذِينَ هَاجَرُوا فِي اللَّهِ مِنْ بَعْدِ مَا ظُلِمُوا لَنُبَوِّئَنَّهُمْ فِي الدُّنْيَا
حَسَنَةً وَلَأَجْرُ الْآخِرَةِ أَكْبَرُ لَوْ كَانُوا يَعْلَمُونَ ﴿41﴾
الَّذِينَ صَبَرُوا وَعَلَىٰ رَبِّهِمْ يَتَوَكَّلُونَ ﴿42﴾ وَمَا أَرْسَلْنَا مِنْ قَبْلِكَ
إِلَّا رِجَالًا نُوحِي إِلَيْهِمْ فَاسْأَلُوا أَهْلَ الذِّكْرِ إِنْ كُنْتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴿43﴾
بِالْبَيِّنَاتِ وَالزُّبُرِ وَأَنْزَلْنَا إِلَيْكَ الذِّكْرَ لِتُبَيِّنَ لِلنَّاسِ مَا نُزِّلَ إِلَيْهِمْ
وَلَعَلَّهُمْ يَتَفَكَّرُونَ ﴿44﴾ أَفَأَمِنَ الَّذِينَ مَكَرُوا السَّيِّئَاتِ
أَنْ يَخْسِفَ اللَّهُ بِهِمُ الْأَرْضَ أَوْ يَأْتِيَهُمُ الْعَذَابُ مِنْ
حَيْثُ لَا يَشْعُرُونَ ﴿45﴾ أَوْ يَأْخُذَهُمْ فِي تَقَلُّبِهِمْ
فَمَا هُمْ بِمُعْجِزِينَ ﴿46﴾ أَوْ يَأْخُذَهُمْ عَلَىٰ تَخَوُّفٍ
فَإِنَّ رَبَّكُمْ لَرَءُوفٌ رَحِيمٌ ﴿47﴾ أَوَلَمْ يَرَوْا إِلَىٰ
مَا خَلَقَ اللَّهُ مِنْ شَيْءٍ يَتَفَيَّأُ ظِلَالُهُ عَنِ
الْيَمِينِ وَالشَّمَائِلِ سُجَّدًا لِلَّهِ وَهُمْ دَاخِرُونَ ﴿48﴾
وَلِلَّهِ يَسْجُدُ مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ
مِنْ دَابَّةٍ وَالْمَلَائِكَةُ وَهُمْ لَا يَسْتَكْبِرُونَ ﴿49﴾
يَخَافُونَ رَبَّهُمْ مِنْ فَوْقِهِمْ وَيَفْعَلُونَ مَا يُؤْمَرُونَ ۩ ﴿50﴾ سجدة

FALALAD HIJRA DA BARAZANA GA KAFIRAI)

41. Wadannan da sukayi hijira (a cikin tsayar da addinin Allah,) bayan an zalunce su (da cuta daga mutanen Makka, sune Annabi Sallallahu alaihi wasallama da sahabbansa) Allah ya yarda dasu, lalle zamu saukar dasu gida kyakkyawa a duniya (Madina.) amma sakamakon Lahira (shine aljanna) shine yafi girma dasun kasance sunsan haka (dasun dace dasu).
42. Sune wadanda suka daure (a Kan cutar mushurikai da hijira don bayyana addini) suke dogara bisa Ubangijinsu, (da sannu zai azurta su inda basa zato.)
43. Bamu aiko gaban ka ba sai mazaje da muke aikowa izuwa garesu (ba Mala'iku ba). Ku tambayi ma'abuta sani (da Attaura da Linjila) in baku san wannan ba, (to, sunsan shi, to, ku kunfi kusa daga gasgata war muminai da Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama.)
44. (Mun aiko su) da hujjoji mabayyana da littattafai, mun saukar da Alƙur'ani a gareka don kayi wa mutane bayanin abinda aka. saukar zuwa garesu (a cikinsa na halal da haram,) donsuyi tunani (cikin wannan suyi lura.)
45. Shin, to, Wadanda suka aikata makirce -makirce (da Annabi Sallallahu alaihi wasallama a gidan shawara na tsare shi ko kashe shi ko fitar dashi,) sun amince Allah ya kisfe ƙasa dasu (tamfar dayayi wa ƙaruna) ko azabatazo musu ta inda basa hasashe, (an halakar dasu a Badar basa zaton wannan.)
46. Ko ya danƙe su a cikin jaurarsu (ta ciniki) su bazasu tsere wa (azabar Allah) ba.
47. Ko ya danƙe su bisa tauyewa (kadan kadan har ya halakar dasu,) haƙiƙa Ubangijinka mai yawan jinƙai ne mai rahama ne (garesu da bai yi musu uƙuba ba.)
48. Basa duba izuwa abinda Allah ya halitta na kowane abu (da yake da inuwa na bishiya da dutse,) inuwoyinsa suna karkacewa ga buransu dama da hauni (farkon rana da ƙarshenta) suna masu sajada ga Allah alhali su suna wulakan -tattu, (an saukar dasu masaukar masu hankali su bishiyoyin Don sun , aikata abinda sai mai hankali ne yake aikatawa.)
49. Abinda yake sammai da ƙassaina daga mai motsi, ga Allah kadai yake sujada, Mala'iku ma suna yi, su basa girman kai (ga buran ibadarsa.)
50. Su wadannan Mala'iku suna tsoron Ubangijinsu daga burbushinsu suna aikata abinda aka umarce su (dashi.)

MUNAƘASHA WATAU BINCIKE-BINCIKE GA MUSHURIKAI A CIKIN AƘIDARSU DA AIKACE AIKACENSU)

حزب

* وَقَالَ اللَّهُ لَا تَتَّخِذُوا إِلَٰهَيْنِ اثْنَيْنِ إِنَّمَا هُوَ إِلَٰهٌ وَاحِدٌ فَإِيَّايَ فَارْهَبُونِ ﴿51﴾
وَلَهُ مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ وَلَهُ الدِّينُ وَاصِبًا أَفَغَيْرَ اللَّهِ تَتَّقُونَ ﴿52﴾
وَمَا بِكُم مِّن نِّعْمَةٍ فَمِنَ اللَّهِ ثُمَّ إِذَا مَسَّكُمُ الضُّرُّ فَإِلَيْهِ تَجْأَرُونَ ﴿53﴾
ثُمَّ إِذَا كَشَفَ الضُّرَّ عَنكُمْ إِذَا فَرِيقٌ مِّنكُم بِرَبِّهِمْ يُشْرِكُونَ ﴿54﴾
لِيَكْفُرُوا بِمَا آتَيْنَاهُمْ فَتَمَتَّعُوا فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ ﴿55﴾ وَيَجْعَلُونَ لِمَا
لَا يَعْلَمُونَ نَصِيبًا مِّمَّا رَزَقْنَاهُمْ تَاللَّهِ لَتُسْأَلُنَّ عَمَّا كُنتُمْ تَفْتَرُونَ ﴿56﴾
وَيَجْعَلُونَ لِلَّهِ الْبَنَاتِ سُبْحَانَهُ وَلَهُم مَّا يَشْتَهُونَ ﴿57﴾ وَإِذَا بُشِّرَ أَحَدُهُم
بِالْأُنثَىٰ ظَلَّ وَجْهُهُ مُسْوَدًّا وَهُوَ كَظِيمٌ ﴿58﴾ يَتَوَارَىٰ مِنَ الْقَوْمِ مِن سُوءِ
مَا بُشِّرَ بِهِ أَيُمْسِكُهُ عَلَىٰ هُونٍ أَمْ يَدُسُّهُ فِي التُّرَابِ أَلَا سَاءَ مَا يَحْكُمُونَ ﴿59﴾
لِلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِالْآخِرَةِ مَثَلُ السَّوْءِ وَلِلَّهِ الْمَثَلُ الْأَعْلَىٰ وَهُوَ الْعَزِيزُ
الْحَكِيمُ ﴿60﴾ وَلَوْ يُؤَاخِذُ اللَّهُ النَّاسَ بِظُلْمِهِم مَّا تَرَكَ عَلَيْهَا مِن دَابَّةٍ
وَلَٰكِن يُؤَخِّرُهُمْ إِلَىٰ أَجَلٍ مُّسَمًّى فَإِذَا جَاءَ أَجَلُهُمْ لَا يَسْتَأْخِرُونَ سَاعَةً
وَلَا يَسْتَقْدِمُونَ ﴿61﴾ وَيَجْعَلُونَ لِلَّهِ مَا يَكْرَهُونَ وَتَصِفُ أَلْسِنَتُهُمُ الْكَذِبَ أَنَّ
لَهُمُ الْحُسْنَىٰ لَا جَرَمَ أَنَّ لَهُمُ النَّارَ وَأَنَّهُم مُّفْرَطُونَ ﴿62﴾ * تَاللَّهِ لَقَدْ أَرْسَلْنَا إِلَىٰ أُمَمٍ
مِّن قَبْلِكَ فَزَيَّنَ لَهُمُ الشَّيْطَانُ أَعْمَالَهُمْ فَهُوَ وَلِيُّهُمُ الْيَوْمَ وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿63﴾

ثمن

51. Ubangiji yace, "Kadaku ,riƙi iyayen giji guda biyu, shi Ubangiji ɗaya ne kawai, ni kaɗai sai ku tsorace ni."
52. Abinda yake sammai da ƙassaina Allah ne (mallaka da halittada bauta,) biyayya na ga Allah tutur, shin to, wanin Allah kuke jin tsoro?
53. Duk abinda ke gareku na ni'ima daga Allah yake, kuma idan talauci da rashin lafiyaya same ku, to, izuwa gareshi zaku daukaka kururuwa (da neman taimako da addu'a.)
54. Sannan idan ya yaye su ga buran ku, sai ga jama'a daga cikinku suna shirkantawa da Ubangijinsu.
55. Donsu kafirtada abinda muka basu (na daga ni'ima,) to, kuji daɗi da tattarar kubisa bautar gumaka, (firgitarwa ne,) da sannu zaku san (ƙarshen wancananka.)
56. Su mushurikai suna sanya rabo ga abinda basu san (yana amfani ko cutarwa ba, wato gumaka,) daga abinda muka azurta musu (na daga hatsi da dabbobi, suna cewa wannan na Allah ne wannan na gumaka ne, mana ki!) Wallahi za a tambaye ku ga ƙagar da kuke wa Allah.
57. Suna sanya 'ya'ya mata ga Allah (suna cewa Mala'iku 'ya'yan Allah ne,) Tsarki ya tabbatarwa Ubangiji ga buran abinda suke riyawa, suna sanya abinda suke marmari (ga kansu; 'ya'ya maza.)
58. Idan an yi wa ɗayansu albishir da 'ya mace, sai fuskarsa ta zama baƙiƙƙirin, alhali yana cike da fushi.
59. Yana buya daga mutanensa, saboda munin abinda akayi masa albishir dashi, shin ya riƙe shine a bisa wulaƙanci, bada kashewa ko ya turbiɗe shi a turbaya? Kai! Wannan hukunci nasu ya munana.
60. Mummunan misali ya tabbata ga waɗanda basu bada gaskiya da ranar Lahira ba, (shine turbide "ya"yansu matada ransu, tareda bukatuwarsu izuwa garesu da aure, [1] misali mafi daukaka yana ga Allah, (shine cewa ba abin bautawa da gaskiya sai shi,) shine mabuwayi (cikin mulkinsa,) gwani (a cikin aikinsa.)
61. Da Allah yana rukon mutane da abinda suka aikata na zaluntar kansu (da sabanni,) bazai bar wani mai motsi a bayan ƙasa ba, sai dai yana jinkirta musu izuwa lokaci abin ambato ne, idan ajalinsu yazo, baza suyi jinkiri (ga buransa ba) sa'a daya. bakuma zasu gabace shi ba.
62. Suna sanyawan abinda suke ki ga Allah, (na daga "ya"ya matada shariki a cikin shugabanci da wulakanta manzanni,) harasansu suna kuta ƙarya wai kyakkyawar makoma tana garesu wurin Allah, kai! Tabbas wutace ta tabbata garesu, su kuma haƙiƙa masu shishshigi ne.

(WANI ABU NA DAGA SHA'ANUNUWAN IKON ALLAH DA NIMOMINSA A GARE MU)

63. Abin mana ki, Wallahi mun aiko manzanni izuwa al'umma dake gabanka, sai shaiɗan ya ƙawata musu. ayyokansu miyagu (suka gdnta kyakkyawa, suka ƙaryata manzanni, shi shaiɗan) shine uban (fakinsu a nan duniya, azaba mai raɗaɗi tana garesu (a ranar Lahira.)

1) Ba shakka Raiyadc haihuwa yana daga binnc "ya"ya da rai - Sanajiy-

وَمَا أَنزَلْنَا عَلَيْكَ الْكِتَابَ إِلَّا لِتُبَيِّنَ لَهُمُ الَّذِي اخْتَلَفُوا فِيهِ وَهُدًى
وَرَحْمَةً لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿64﴾ وَاللَّهُ أَنزَلَ مِنَ السَّمَاءِ مَاءً فَأَحْيَا بِهِ الْأَرْضَ بَعْدَ
مَوْتِهَا إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَآيَةً لِّقَوْمٍ يَسْمَعُونَ ﴿65﴾ وَإِنَّ لَكُمْ فِي الْأَنْعَامِ لَعِبْرَةً
نَّسْقِيكُم مِّمَّا فِي بُطُونِهِ مِن بَيْنِ فَرْثٍ وَدَمٍ لَّبَنًا خَالِصًا سَائِغًا لِّلشَّارِبِينَ ﴿66﴾
وَمِن ثَمَرَاتِ النَّخِيلِ وَالْأَعْنَابِ تَتَّخِذُونَ مِنْهُ سَكَرًا وَرِزْقًا حَسَنًا إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَآيَةً
لِّقَوْمٍ يَعْقِلُونَ ﴿67﴾ وَأَوْحَىٰ رَبُّكَ إِلَى النَّحْلِ أَنِ اتَّخِذِي مِنَ الْجِبَالِ بُيُوتًا وَمِنَ الشَّجَرِ
وَمِمَّا يَعْرِشُونَ ﴿68﴾ ثُمَّ كُلِي مِن كُلِّ الثَّمَرَاتِ فَاسْلُكِي سُبُلَ رَبِّكِ ذُلُلًا يَخْرُجُ
مِن بُطُونِهَا شَرَابٌ مُّخْتَلِفٌ أَلْوَانُهُ فِيهِ شِفَاءٌ لِّلنَّاسِ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَآيَةً
لِّقَوْمٍ يَتَفَكَّرُونَ ﴿69﴾ وَاللَّهُ خَلَقَكُمْ ثُمَّ يَتَوَفَّاكُمْ وَمِنكُم مَّن يُرَدُّ
إِلَىٰ أَرْذَلِ الْعُمُرِ لِكَيْ لَا يَعْلَمَ بَعْدَ عِلْمٍ شَيْئًا إِنَّ اللَّهَ عَلِيمٌ قَدِيرٌ ﴿70﴾
ربع
* وَاللَّهُ فَضَّلَ بَعْضَكُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ فِي الرِّزْقِ فَمَا الَّذِينَ فُضِّلُوا
بِرَادِّي رِزْقِهِمْ عَلَىٰ مَا مَلَكَتْ أَيْمَانُهُمْ فَهُمْ فِيهِ سَوَاءٌ
أَفَبِنِعْمَةِ اللَّهِ يَجْحَدُونَ ﴿71﴾ وَاللَّهُ جَعَلَ لَكُم مِّنْ أَنفُسِكُمْ أَزْوَاجًا
وَجَعَلَ لَكُم مِّنْ أَزْوَاجِكُم بَنِينَ وَحَفَدَةً وَرَزَقَكُم مِّنَ
الطَّيِّبَاتِ أَفَبِالْبَاطِلِ يُؤْمِنُونَ وَبِنِعْمَتِ اللَّهِ هُمْ يَكْفُرُونَ ﴿72﴾

64. Bamu saukar da Alƙur'ani a gareka ba (Ya Annabi Muhammadu, tsiran Allah ya tabbata a gareka,) sai donka bayyanawa mutane abinda suke saɓani a kansa (a cikin addini,) kuma don shiriya da jinƙai ga mutanen da suka bada gaskiya (dashi.)
65. Allah ne ya sauko da ruwa daga sama, ya raya ƙasa dashi (da iri bayan ƙeƙashewarta, haƙiƙa akwai aya a cikin wancananka (abin ambato, wato alama mai shiryarwa a kan tashin alƙiyama.) ga mutane masuji don lura.
66. Haƙiƙa kuna da izna a cikin dab-bobi.Muna shayar daku ,nono tacacce daga ɗanɗani ko Kanshi ko kuma daga abinda yake cikin cukkunanta daga tsakanin tuka da jini, mai kwarara a makogwaro ga masu sha.
67. Akwai dan Itace daga "ya"yayen dabinai da inabai da kuke riƙo giya daga gareshi, (wannan gaban haramtata ne, wato nannagangen inabi wanda baya sa maye,) da arziki kyakkyawa, (kamar dabino da zabibi da madi,) haƙiƙa akwai aya (mai shiryarwa bisa girman Ubangiji) a cikin wancananka ga mutane masu hankali. (RUDAN ZUMA DA MANA KANTA)
68. Ubangijinka ya aiko izuwa ƙudanzuma (aike na ilhama) cewa ki riƙi ɗakuna daga du-warwatsu, daza ki tattara izuwa gareta haka kuma ki riƙi daga itatuwa kuma ki riƙi daga abinda ake jera miki (na daga guraran zama, kamar amya.)
69. Sannan kici daga dukkan "ya"yan itatuwa ki shiga hanyar Ubangijinki (a cikin neman makiyaya,) abar horewa (gareki, bazata wuyata gareki ba, komai wuyarta, baza ki ɓata ga buran komowa daga gareta ba komai nisanta,) abin sha yana fitowa daga cukkunanta (shine zuma,) mai sassaɓawar launinsa, akwai waraka ga mutane a cikinsa (daga dukkan cutuka, haƙiƙa Manzon Allah mai tsira da aminci, ya umarci wanda cikinsa ya sakuda shan zuma, Buhari da Muslim sun ruwa ito shi.) Akwai aya cikin wancananka ga mutane masu tunani (cikin aikin Allah.)

(WANI ABU DAGA MANA KAN IKON ALLAH DA AYOYIN KADAITAKA TASA)

70. Ubangiji ne ya halicce ku alhali bakuna komai ba, sannan ya karɓi ranku (yayin ƙarewan ajalin ku,) akwai daga gareku wanda ake komo dashi izuwa mafi wulakancin rayuwa, (tsufa da rikicewa don kada ya san komai bayan saninsa, (Ikrimatu yace wanda ya karanta Alƙur'ani bazai zama haka ba [1] haƙiƙa Mayarwa izuwa Arzalil umuri ya kan zama ne ga kafirai da masu kutsawa acikin bin sha, awaice - sha'awaice na daga tarkacen musulmi INTAHA "SAWI". Ubangiji masanine (dashirin halitta) mai iko ne (bisa abinda yake nufi.)
71. Ubangiji yafifita shashin kubisa shashi a cikin arziki, (akwai mawadaci da talaka daga cikin kuda bawa da ubangiji,) to, waɗannan da aka fifita su su shiyagabanni basu kasance masu mai da arzikinsu a kan abinda hannunsu ta mallaka ba, (wato su zama masu tarayya tsakaninsu da bayinsu.) to, yanzu su, bayin nan dashiyagaban-ni daidai suke a cikin abinda suka mallaka? (A'a! basuyi tarayya da bayinsu a cikin abinda suka mallaka ba, to, ƙaƙa zasu sanya ba'alin abin mallakar Ubangiji sharikai a gareshi.) Shin, da ni'imar Allah suke butulcewa?
72. Allah ne yasanya muku mataye daga kawukanku (ya halicci Nana Hauwa'u daga autan haƙarƙarin Annabi Adamu tsira da aminci ya tabbata a gareshi, Ya halicci sauran mataye daga ruwan mazaje da mataye,) Yasanya muku 'ya'ya da jikoki daga matayen ku, ya azurta ku daga daɗaɗa (na daga nau'o'in itatuwa da kwayuka da dabbobi,) Shin, to da ƙarya (gunki) suke bada gaskiya, da ni'imar Allah suke butulcewa?

1) "sawi" yace ai wanda yayi aiki dashi hakana malamai masu aiki da ilminsu suma basa zama haka,dukkan, sanda suka kara a cikin shekaru, saisu kara ilimi da sanin Allah da hankali, (gani yakorgi,) don haka suke cewa mafi daukakar zancen masana Allah abinda suka faɗa a ƙarshen ransu.

وَيَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَمْلِكُ لَهُمْ رِزْقًا
مِّنَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ شَيْـًٔا وَلَا يَسْتَطِيعُونَ ﴿٧٣﴾
فَلَا تَضْرِبُوا۟ لِلَّهِ ٱلْأَمْثَالَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ وَأَنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴿٧٤﴾
ضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلًا عَبْدًا مَّمْلُوكًا لَّا يَقْدِرُ عَلَىٰ شَىْءٍ
وَمَن رَّزَقْنَٰهُ مِنَّا رِزْقًا حَسَنًا فَهُوَ يُنفِقُ مِنْهُ سِرًّا وَجَهْرًا ۖ
هَلْ يَسْتَوُۥنَ ۚ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ۚ بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٧٥﴾
وَضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلًا رَّجُلَيْنِ أَحَدُهُمَآ أَبْكَمُ لَا يَقْدِرُ عَلَىٰ شَىْءٍ
وَهُوَ كَلٌّ عَلَىٰ مَوْلَىٰهُ أَيْنَمَا يُوَجِّههُّ لَا يَأْتِ بِخَيْرٍ ۖ
هَلْ يَسْتَوِى هُوَ وَمَن يَأْمُرُ بِٱلْعَدْلِ ۙ وَهُوَ عَلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿٧٦﴾
وَلِلَّهِ غَيْبُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ وَمَآ أَمْرُ ٱلسَّاعَةِ إِلَّا كَلَمْحِ
ٱلْبَصَرِ أَوْ هُوَ أَقْرَبُ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٧٧﴾
وَٱللَّهُ أَخْرَجَكُم مِّنۢ بُطُونِ أُمَّهَٰتِكُمْ لَا تَعْلَمُونَ شَيْـًٔا
وَجَعَلَ لَكُمُ ٱلسَّمْعَ وَٱلْأَبْصَٰرَ وَٱلْأَفْـِٔدَةَ ۙ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿٧٨﴾
* أَلَمْ يَرَوْا۟ إِلَى ٱلطَّيْرِ مُسَخَّرَٰتٍ فِى جَوِّ ٱلسَّمَآءِ مَا يُمْسِكُهُنَّ ثمن
إِلَّا ٱللَّهُ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿٧٩﴾

73. Suna bautawa daga wanin Allah abinda bai mallaki arzikin wani abu bana daga sammai da ƙassaida ruwa da ƙasa (da tsiri) basu da iko a bisa komai (sune gumaka.)
74. To, ku daina sanya misalcemisalce ga Allah, haƙiƙa Allah yasan (bashi da tamka,) amma ku baku san (wannan ba!)

(MISALIN GUMAKA DA DODANNI)

75. Ubangiji yasanya misali, bawa abin mallaka da bashi da iko bisa komai, da wanda muka azurta masa arziki kyakkyawa daga garemu, shi yana ciyarwa daga gareshi a asirce da bayyane sayi daidai, (wato bayin nan azurta ttu da da mai tasarrufi, a'a, baza suyi daidai ba,)Godiya ta tabbata ga Allah, Kai! yawancinsu basu san (ƙarshen al'amannsu ba.)
76. Allah yasanya misali, mutum biyu, ɗayansu bebe ne, bashi da iko bisa komai, shi nauyi ne a bisa uban ɗakinsa, inda duk ya fuskantar dashi bazai zoda alhcri ba, zai daidai da wanda yake umarni da adalci, shi yana kan tafarki madaidaici (wato shine mumini, baza suyi daidai ba.)
77. Abinda ya faku na sammai da ƙassaina Allah ne, al'amarin alƙiyama bai kasance ba illa kamar ƙiftawar idanu ko mafi hanzari daga gareshi, haƙiƙa Ubangiji mai iko ne bisa komai.
78. Ubangiji ne yafito daku ,daga cukkunan iyayen ku mataye baku san komai ba, yasanya muku kunnuwa da idanduna da zukata don ku gode masa (ku bada gaskiya.)
79. Yanzu basuyi duba izuwa tsuntsaye ba ababan horewa a cikin sama, ba abinda yake riƙe su (yayin ɗauke fikafikansu dayayin shinfiɗe ta, ba abinda ya riƙe su) sai Allah [1]. Haƙiƙa akwai ayoyi a cikin wancananka ga mutane da suka bada gaskiya.

1) Jirgin sama yana daga cikinsu da makamancinsa Sanajiy

وَاللَّهُ جَعَلَ لَكُم مِّنۢ بُيُوتِكُمْ سَكَنًا وَجَعَلَ لَكُم مِّن جُلُودِ
الْأَنْعَامِ بُيُوتًا تَسْتَخِفُّونَهَا يَوْمَ ظَعْنِكُمْ وَيَوْمَ إِقَامَتِكُمْ
وَمِنْ أَصْوَافِهَا وَأَوْبَارِهَا وَأَشْعَارِهَا أَثَاثًا وَمَتَاعًا إِلَىٰ حِينٍ ﴿80﴾
وَاللَّهُ جَعَلَ لَكُم مِّمَّا خَلَقَ ظِلَالًا وَجَعَلَ لَكُم مِّنَ الْجِبَالِ
أَكْنَانًا وَجَعَلَ لَكُمْ سَرَابِيلَ تَقِيكُمُ الْحَرَّ وَسَرَابِيلَ تَقِيكُم
بَأْسَكُمْ كَذَٰلِكَ يُتِمُّ نِعْمَتَهُ عَلَيْكُمْ لَعَلَّكُمْ تُسْلِمُونَ ﴿81﴾
فَإِن تَوَلَّوْا فَإِنَّمَا عَلَيْكَ الْبَلَاغُ الْمُبِينُ ﴿82﴾ يَعْرِفُونَ نِعْمَتَ اللَّهِ
ثُمَّ يُنكِرُونَهَا وَأَكْثَرُهُمُ الْكَافِرُونَ ﴿83﴾ وَيَوْمَ نَبْعَثُ
مِن كُلِّ أُمَّةٍ شَهِيدًا ثُمَّ لَا يُؤْذَنُ لِلَّذِينَ
كَفَرُوا وَلَا هُمْ يُسْتَعْتَبُونَ ﴿84﴾ وَإِذَا رَأَى الَّذِينَ
ظَلَمُوا الْعَذَابَ فَلَا يُخَفَّفُ عَنْهُمْ وَلَا هُمْ يُنظَرُونَ ﴿85﴾
وَإِذَا رَأَى الَّذِينَ أَشْرَكُوا شُرَكَاءَهُمْ قَالُوا
رَبَّنَا هَٰؤُلَاءِ شُرَكَاؤُنَا الَّذِينَ كُنَّا نَدْعُوا مِن دُونِكَ
فَأَلْقَوْا إِلَيْهِمُ الْقَوْلَ إِنَّكُمْ لَكَاذِبُونَ ﴿86﴾ وَأَلْقَوْا إِلَى
اللَّهِ يَوْمَئِذٍ السَّلَمَ وَضَلَّ عَنْهُم مَّا كَانُوا يَفْتَرُونَ ﴿87﴾

(WANI ABU NA NFIMOMIN ALLAH A GAREMU)

80. Ubangiji yasanya ipuku mazauni daga ɗakunan ku, yasanya muku ɗakuna daga fatun nan na dabbobi (kamar haimomi da ƙubbobi da gubbobi) ku ke jin sauƙin ɗaukarta ranar tafiyar kuda ranar zaman ku, ya halarta muku daga (gashin tumakantada gasun rakumantada gasun awa kanta dan jin daɗi ga ɗakunanku, da Jikin kuda jindaɗi izuwa ƙarewar ajalin ku.

81. Ubangiji ne yasanya muku inuwai daga abinda ya halitta (na daga ɗakuna itatuwa da gizagizai) yasanya muku guraran shiga daga duwarwatsu da kogwanni da ɗakunan ƙasa, yasanya muku riguna dake kiyaye ku (sanyi) da zafi, da riguna da take kiyaye ku yaƙin ku (kamar sulke da garkuwanni,) tamfar daya halicci waɗannan abubuwa yake cika ni'imarsa a gareku don ku kaɗaita shi.

82. Idan suka bujira ga buran Musulunci, to, kawai ida aike ne mabayyani yake kanka (tsira da amincin Allah ya tabbata a gareka.) Wannan tun gaban umarni dayaki ne.

83. Sunsan ni'imar Allah (cewa ita daga gareshi take,) sannan suna musun ta (da mushirikancinsu,) yawaicinsu kafirai ne.

(MATSAYI DAGA MATSAYAN RANAR ALƘIYAMA)

84. Ka ambaci ranar da muke taso mai shaida daga kowace al'umma (shine Annabinta dazai shaida matada alheri ko kishiyarta, Itace ranar Alƙiyama,) sannan baza ayi izini ga waɗanda suka kafirta (a cikin yin hanzari ba) bakuma za a nemi komawarsu (izuwa ɗa'a ba.)

85. Idan waɗanda suka kafirta sun ga azaba, to, baza a saukake musu azabar wuta ba, bakuma za a saurara musu ba.

86. Idan mushirikai suka ga abokansu na shaiɗanu (da waninsu,) saisu ce "Ya Ubangijinmu waɗannan sune abokanmu waɗanda muke bautawa bakai ba" Sai suka kada baki, sukace (dasu,) " Haƙiƙa ku, maƙaryata ne (a cikin maganar ku cewa ku kunbautamana".)

87. Suka maida jawuwa izuwa Allah a wannan rana, abinda suke ƙirƙira (na cewa gumaka za tacece su) ya bace ga buran su.

ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ زِدْنَٰهُمْ عَذَابًا
فَوْقَ ٱلْعَذَابِ بِمَا كَانُواْ يُفْسِدُونَ ﴿88﴾ وَيَوْمَ نَبْعَثُ فِي كُلِّ
أُمَّةٍ شَهِيدًا عَلَيْهِم مِّنْ أَنفُسِهِمْ وَجِئْنَا بِكَ شَهِيدًا عَلَىٰ
هَٰٓؤُلَآءِ وَنَزَّلْنَا عَلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ تِبْيَٰنًا لِّكُلِّ شَيْءٍ وَهُدًى
وَرَحْمَةً وَبُشْرَىٰ لِلْمُسْلِمِينَ ﴿89﴾ * إِنَّ ٱللَّهَ يَأْمُرُ بِٱلْعَدْلِ ربع
وَٱلْإِحْسَٰنِ وَإِيتَآيِٕ ذِي ٱلْقُرْبَىٰ وَيَنْهَىٰ عَنِ ٱلْفَحْشَآءِ
وَٱلْمُنكَرِ وَٱلْبَغْيِ يَعِظُكُمْ لَعَلَّكُمْ تَذَّكَّرُونَ ﴿90﴾ وَأَوْفُواْ
بِعَهْدِ ٱللَّهِ إِذَا عَٰهَدتُّمْ وَلَا تَنقُضُواْ ٱلْأَيْمَٰنَ بَعْدَ
تَوْكِيدِهَا وَقَدْ جَعَلْتُمُ ٱللَّهَ عَلَيْكُمْ كَفِيلًا إِنَّ ٱللَّهَ
يَعْلَمُ مَا تَفْعَلُونَ ﴿91﴾ وَلَا تَكُونُواْ كَٱلَّتِي نَقَضَتْ غَزْلَهَا
مِنۢ بَعْدِ قُوَّةٍ أَنكَٰثًا تَتَّخِذُونَ أَيْمَٰنَكُمْ دَخَلًا بَيْنَكُمْ
أَن تَكُونَ أُمَّةٌ هِيَ أَرْبَىٰ مِنْ أُمَّةٍ إِنَّمَا يَبْلُوكُمُ ٱللَّهُ بِهِۦ
وَلَيُبَيِّنَنَّ لَكُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ مَا كُنتُمْ فِيهِ تَخْتَلِفُونَ ﴿92﴾
وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ لَجَعَلَكُمْ أُمَّةً وَٰحِدَةً وَلَٰكِن يُضِلُّ مَن يَشَآءُ
وَيَهْدِي مَن يَشَآءُ وَلَتُسْـَٔلُنَّ عَمَّا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿93﴾

88. Waɗanda suka kafirta suka hana mutane ga buran bin addinin Allah, zamu kara musu azaba burbushin azaba (wacce suka cancance ta, Ibn Mas'udu yace kunami ne waɗanda ƙirorinsu kamar dogwayen dabinai) ne saboda kasancewar su suna ɓarna.

89. Kuma ka ambaci zamanin da muke zuwa da mai shaida a kan kowace al'umma na daga kawu-kansu (shine Annabinsu,) muka zodakai (tsira da amincin Allah ya tabbata a gareka,) shaida a kan waɗannan (wato mutanenka,) muka saukar da Alƙur'ani a gareka, don bayani ga kowane abu (da ake bukata izuwa gareshi na daga lamarin addini.) dashiryarwa (daga ɓata,) da raha-ma da gargaɗi (da aljanna) ga Musulmai.

(MAFI TATTARAWAN AYAGA HAIRI DA SHARRI)

90. Haƙiƙa Ubangiji yana umarni da adalci yana umarni da sanin sa na yaƙini, (wato ka bautawa Allah kamar kana ganinsa, tamfar yadda yazo a hadisi,) da baiwa ma'abuta zumunta, yana hani ga buran alfasha, (zina,) da abin musu ga shari'a (kafirci da sabo da zalunci) ga mutane, yanayi muku wa'azi (amru da nahyu,) don ku wa'azantu.

HARAM CIN WAR WARE AL ƘAWARI KAMAR FITA DAGA DARIƘA

91. Ku cika da alƙawarin Allah, (na ciniki da rantse- rantse da wanin su) idan kun yi alƙawari, kadaku ,warware rantse-rantse bayan ƙarfafa ta, alhali kun sanya Ubangiji wakili a kanku, (da kuka rantse dashi a kan cika alƙawari,) haƙiƙa Allah yasan abindaku ,ke aikatawa, (firgitarwa ne garesu).

92. Kadaku ,kasance kamar matanan data warware Kaɗinta bayan ingantashi, a warware, kuna riƙon rantserantsen ku shigogo a tsakanin ku, (wato ɓarna da zambashine ku warware ta) don wata al'umma ta kasance mafi yawa daga wata al'umma. (Sun kasance suna rantsuwa da abokan rantsuwarsu idan suka sami mafi yawa daga garesu,) haƙiƙa Ubangiji yana jarrabakune dashi (abinda ya umarce ku na cika alƙawarin nan don yaga mai bi da mai sabo,) kuma lalle zai bayyana A gareku ramar Alƙiyama a duniya daga lamarin alƙawari da waninsa agareku anan alƙiyama da waninsa ya azabci mai war ware alƙawari yashigar da mai cikawa Aljanna abinda kuka kasance kuna sassaɓawa a cikinsa.

93. Da Allah yaso da saiya mai daku ,al'umma guda ɗaya, masu addini daya sai dai yana ɓatar da wanda yaga dama yana shiryar wanda yaga dama. Lalle Wallahi za a tambaye ku ga abinda kuka kasance kuna aikatawa, (irin tambaya ta zargi don ayi muku sakamako a kai.)

وَلَا تَتَّخِذُوٓاْ أَيۡمَٰنَكُمۡ دَخَلَۢا بَيۡنَكُمۡ فَتَزِلَّ قَدَمُۢ بَعۡدَ ثُبُوتِهَا
وَتَذُوقُواْ ٱلسُّوٓءَ بِمَا صَدَدتُّمۡ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلَكُمۡ
عَذَابٌ عَظِيمٞ 94 وَلَا تَشۡتَرُواْ بِعَهۡدِ ٱللَّهِ ثَمَنٗا قَلِيلًاۚ
إِنَّمَا عِندَ ٱللَّهِ هُوَ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ 95
مَا عِندَكُمۡ يَنفَدُ وَمَا عِندَ ٱللَّهِ بَاقٖ وَلَيَجۡزِيَنَّ ٱلَّذِينَ صَبَرُواْ
أَجۡرَهُم بِأَحۡسَنِ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ 96 مَنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا
مِّن ذَكَرٍ أَوۡ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَلَنُحۡيِيَنَّهُۥ حَيَوٰةٗ طَيِّبَةٗ
وَلَنَجۡزِيَنَّهُمۡ أَجۡرَهُم بِأَحۡسَنِ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ 97
* فَإِذَا قَرَأۡتَ ٱلۡقُرۡءَانَ فَٱسۡتَعِذۡ بِٱللَّهِ مِنَ ٱلشَّيۡطَٰنِ ٱلرَّجِيمِ 98 ثمن
إِنَّهُۥ لَيۡسَ لَهُۥ سُلۡطَٰنٌ عَلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَلَىٰ رَبِّهِمۡ
يَتَوَكَّلُونَ 99 إِنَّمَا سُلۡطَٰنُهُۥ عَلَى ٱلَّذِينَ يَتَوَلَّوۡنَهُۥ
وَٱلَّذِينَ هُم بِهِۦ مُشۡرِكُونَ 100 وَإِذَا بَدَّلۡنَا ءَايَةٗ مَّكَانَ ءَايَةٖ
وَٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِمَا يُنَزِّلُ قَالُوٓاْ إِنَّمَا أَنتَ مُفۡتَرِۭ بَلۡ أَكۡثَرُهُمۡ
لَا يَعۡلَمُونَ 101 قُلۡ نَزَّلَهُۥ رُوحُ ٱلۡقُدُسِ مِن رَّبِّكَ بِٱلۡحَقِّ
لِيُثَبِّتَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَهُدٗى وَبُشۡرَىٰ لِلۡمُسۡلِمِينَ 102

94. Kadaku ,riƙi Rantse rantsen ku shigogo (ko tomo tsakanin ku) sai dunduniyar ku ta zame (ga buran doran hanyar Musulunci,) bayan ta tabbata, ku ɗanɗani azaba don kun tsare ga buran hanyar Allah da cika alƙawari, azaba mai girma tana gareku (a ranar Lahira.)
95. Kadaku ,sayo dan tamani kankane da alƙawarin Allah, haƙiƙa abinda yake gun Allah (na sakamako) shine yafi gare ku, in kun kasance kun san (wannan to, kadaku ,warware alƙawari.)
96. Abinda yake gun Ku (na duniya) ƙarewa zai yi, abinda yake wurin Ubangiji mai dauwama ne, Lalle Allah zai saka wa waɗanda sukayi haƙuri sakamakonsu da kyakkyawan abinda suka aikata.
97. Wanda yayi aiki nagari na miji ko mace alhali yana mumini, Lalle zamu raya shi rayuwa daddaɗa a Lahira, lalle- zamu saka musu sakamakonsu da kyakkyawan abinda suka kasance suna aikatawa.

(WANI ABU DAGA LADABAN ALƘUR'ANI DA FUSKANTARWARSA)

98. In zaka karanta wani abu daga Alƙur'ani ka nemi tsari da shaiɗan abin nisantawa daga rahamar Allah.

KACE A'UZU BILLAHI MINAS SHAIDANIR RAJIM

99. Haƙiƙa shi, bashi da kataɓus a kan waɗanda suka bada gaskiya sukayi dogaro bisa Ubangijinsu.
100. Kuzarinsa dai a kan waɗanda suka jibince shine kawai da waɗanda suke masu shirka da Allah.
101. Idan muka musanya wata aya maimakon wata aya (muka shafe ta,) muka saukar da wata maimakon ta, (saboda masalahar ga bayi,) Allah ne masani da abinda yake saukarwa, sai kafirai su ce "Da Ma'aiki (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi,) " Haƙiƙa kai dai mai ƙirƙira ne kawai, (kana kuta shine daga gareka") bari! yawaicin su basu san (haƙiƙa r ALƙur'ani ba ba, su san kuma amfanin shafe ayar sa ba.)
102. Cene (dasu) Mala'ika jibrilu tsira da amincin Allah ya tabbata a g areshine ya saukar dashi daga Ubangijin ka, da gaskiya domin ya tabbatar da waɗanda suka bada gaskiya, (wato suka bada gaskiya dashi,) shinya ne da albishir ga Musulmi.

وَلَقَدْ نَعْلَمُ أَنَّهُمْ يَقُولُونَ إِنَّمَا يُعَلِّمُهُۥ بَشَرٌۗ
لِّسَانُ ٱلَّذِي يُلْحِدُونَ إِلَيْهِ أَعْجَمِيٌّ وَهَٰذَا لِسَانٌ
عَرَبِيٌّ مُّبِينٌ ﴿103﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ
لَا يَهْدِيهِمُ ٱللَّهُ وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿104﴾ إِنَّمَا يَفْتَرِي
ٱلْكَذِبَ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ
هُمُ ٱلْكَٰذِبُونَ ﴿105﴾ مَن كَفَرَ بِٱللَّهِ مِنۢ بَعْدِ
إِيمَٰنِهِۦٓ إِلَّا مَنْ أُكْرِهَ وَقَلْبُهُۥ مُطْمَئِنٌّۢ بِٱلْإِيمَٰنِ
وَلَٰكِن مَّن شَرَحَ بِٱلْكُفْرِ صَدْرًا فَعَلَيْهِمْ غَضَبٌ
مِّنَ ٱللَّهِ وَلَهُمْ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿106﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمُ
ٱسْتَحَبُّواْ ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَا عَلَى ٱلْأٓخِرَةِ وَأَنَّ ٱللَّهَ
لَا يَهْدِي ٱلْقَوْمَ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿107﴾ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ طَبَعَ ٱللَّهُ
عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ وَسَمْعِهِمْ وَأَبْصَٰرِهِمْۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْغَٰفِلُونَ ﴿108﴾
لَا جَرَمَ أَنَّهُمْ فِي ٱلْأٓخِرَةِ هُمُ ٱلْخَٰسِرُونَ ﴿109﴾ ثُمَّ إِنَّ رَبَّكَ
لِلَّذِينَ هَاجَرُواْ مِنۢ بَعْدِ مَا فُتِنُواْ ثُمَّ جَٰهَدُواْ
وَصَبَرُوٓاْ إِنَّ رَبَّكَ مِنۢ بَعْدِهَا لَغَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿110﴾

103. Hakika mu, mun sani cewa su lalle suna cewa mutumne yake sanar dashi (wannan Alkur'ani, suna nufin wani makeri Banasare, ya kasance yana zuwa wurin Annabi mai tsira da aminci, sai Ubangiji yace,) "Yaren wadanda . suke karkata izuwa gareshi cewa shine yake ganar da manzon Allah Shi yake sanar dashi na Baibayi ne, wannan ALkur'ani kuwa yare ne Balarabe mabayyanin fasaha ba gargaliya, (kaka Baubawa zai sanar dashi?")

104. Hakika wadanda basu bada gaskiya da ayoyin Allah ba, Allah bazai shiryesu ba. Azaba mai radadi na garesu.

105. Wadanda basu bada gaskiya da Allah basune suke kirkirar karya (da cewa wannan Alkur'ani kirkirar bawa ne,) wancananka sune hakika r makaryata.

(MASU RIDDA GA BURAN MUSULUNCI ALLAH YA KIYASHE MU AMIN)

106. Wanda ya kafirtada Allah bayan imaninsa, sai wanda aka tilashe shi (a kan kalmar kafirci yayi ta bisa tilas) alhali zuciyarsa tana cikin nutsuwa da imani, (narko mai tsanani ya tabbata gareshi,) amma wadanda kirjinsu yayi sarari da kafirci, to, azabar Allah ce garesu, azaba mai girma tana garesu.

107. Wancananka (narko garesu,) saboda cewa hakika su, sun fifita rayuwar duniya a kan Lahira, hakika Ubangiji baya shiriyar mutane kafirai.

108. Wadancananka sune wadanda Allah ya yimke bisa zukatansu da kunnuwansu da idanuwansu, wadancananka hakika sune marabkana.

109. Ba shakka su sune hakika r tababbu a ranar Lahira, (saboda komawar su izuwa wuta abar dauwama garesu.)

110. Sannan hakika Ubangijinka mai gafara ne mai jinkai ga wadannan da sukayi kaura (izuwa Madina(bayan an azabce su, sannan sukayi yaki suka daure (bisa bin Allah,) hakika Ubangijinka bayan wancananka mai gafara ne mai jinkai (a garesu.)

ربع

۞ يَوۡمَ تَأۡتِي كُلُّ نَفۡسٖ تُجَٰدِلُ عَن نَّفۡسِهَا وَتُوَفَّىٰ كُلُّ نَفۡسٖ مَّا عَمِلَتۡ
وَهُمۡ لَا يُظۡلَمُونَ ١١١ وَضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلٗا قَرۡيَةٗ كَانَتۡ
ءَامِنَةٗ مُّطۡمَئِنَّةٗ يَأۡتِيهَا رِزۡقُهَا رَغَدٗا مِّن كُلِّ مَكَانٖ
فَكَفَرَتۡ بِأَنۡعُمِ ٱللَّهِ فَأَذَٰقَهَا ٱللَّهُ لِبَاسَ ٱلۡجُوعِ وَٱلۡخَوۡفِ
بِمَا كَانُواْ يَصۡنَعُونَ ١١٢ وَلَقَدۡ جَآءَهُمۡ رَسُولٞ مِّنۡهُمۡ فَكَذَّبُوهُ
فَأَخَذَهُمُ ٱلۡعَذَابُ وَهُمۡ ظَٰلِمُونَ ١١٣ فَكُلُواْ مِمَّا رَزَقَكُمُ ٱللَّهُ
حَلَٰلٗا طَيِّبٗا وَٱشۡكُرُواْ نِعۡمَتَ ٱللَّهِ إِن كُنتُمۡ إِيَّاهُ
تَعۡبُدُونَ ١١٤ إِنَّمَا حَرَّمَ عَلَيۡكُمُ ٱلۡمَيۡتَةَ وَٱلدَّمَ وَلَحۡمَ ٱلۡخِنزِيرِ
وَمَآ أُهِلَّ لِغَيۡرِ ٱللَّهِ بِهِۦۖ فَمَنِ ٱضۡطُرَّ غَيۡرَ بَاغٖ وَلَا عَادٖ فَإِنَّ ٱللَّهَ
غَفُورٞ رَّحِيمٞ ١١٥ وَلَا تَقُولُواْ لِمَا تَصِفُ أَلۡسِنَتُكُمُ ٱلۡكَذِبَ
هَٰذَا حَلَٰلٞ وَهَٰذَا حَرَامٞ لِّتَفۡتَرُواْ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَۚ
إِنَّ ٱلَّذِينَ يَفۡتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَ لَا يُفۡلِحُونَ ١١٦
مَتَٰعٞ قَلِيلٞ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ١١٧ وَعَلَى ٱلَّذِينَ
هَادُواْ حَرَّمۡنَا مَا قَصَصۡنَا عَلَيۡكَ مِن قَبۡلُۖ
وَمَا ظَلَمۡنَٰهُمۡ وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ١١٨

111. Ranar da kowacc kai take jayayyaga buran kanta, ake cikawa kowace kai abindata aikata, su baza a zalunce su komai ba.

(AƘIBAR WANDA YA BUTULCE NFIMA)

112. Ka sanya musu misalin alƙarya (Makka ai mutanenta,) ta kasance amintacciya (daga harehare, ba a firgita ta, tana cikin kwanciyar hankali, bata bukatar curuwa izuwa wani wuri,) arzikinta yana zuwa mata mayalwaci daga kowane wuri, ta butulce da ni'imomin Ubangiji (saboda ƙaryatawar tada Ma'aikin ALlah mai tsira da amincin ALlah,) saboda haka sai Ubangiji ya ɗanɗana mata tufan yinwa (akayi musu fari shekara bakwai, da tufar tsoro da harehare na Manzon Allah, mai tsira da amincin Allah) saboda abinda suka kasance suna aikatawa.
113. Haƙiƙa Manzo daga cikinsu yazo musu (Annabi mai tsira da amincin Allah) suka ƙi gasgatawa dashi, sai azabar yinwa da tsoro ta kama su, alhali suna azzalumai.
114. To, Kuci (Yaku muminai) daga abinda muka halarta muku, Kuci daga abu daddaɗa ku godewa ni'imar Allah in kun kasance shi kaɗai ku ke bautawa.
115. Haƙiƙa dai ya haramta muku mushe ne kawai da jini da naman alade da abinda aka ambaci sunan wanin Allah (yayin yankan sa,) to, duka wanda aka buƙatar dashi ba yana ɗan tawaye ba ba yana mai shisshigi ba, haƙiƙa Ubangiji mai gafara ne mai rahama (a gareshi.)
116. Kadaku ,faɗa saboda su ffantawar harasan ku ƙarya, "wannan halal ne wannan haram ne" (daga abinda Allah bai haramta shi ba, ko halitta shi) sabodaku ,ƙagi ƙarya bisa Allah, (da dangana wancananka ƙarya a gareshi,) haƙiƙa waɗannan dasuke ƙagen ƙaryaga Allah bazasu tsira ba.
117. Don amfani ƙanƙani na duniya (ya tabbata garesu,) azaba mai raɗaɗi ta tabbata a garesu a Lahira.

(BINCIKE-BINCIKEN MUSHIRIKAI CIKIN KUDIRE-KUDIRENSU)

118. Mun haramta abinda muka labarta maka tun can gaba, ga waɗannan da suka zama Yahudu, (shine haramcin dukkan ma'abucin farcc,) bamu zalunce su ba (da haramta wancananka) sune suka zalunci kawukansu (da zaikewa saɓanni wacce take wajabta wancananka.)

ثُمَّ إِنَّ رَبَّكَ لِلَّذِينَ عَمِلُواْ اُ۬لسُّوٓءَ بِجَهَٰلَةٖ ثُمَّ تَابُواْ مِنۢ
بَعْدِ ذَٰلِكَ وَأَصْلَحُوٓاْ إِنَّ رَبَّكَ مِنۢ بَعْدِهَا لَغَفُورٞ رَّحِيمٌ ﴿119﴾
ثمن
۞ إِنَّ إِبْرَٰهِيمَ كَانَ أُمَّةٗ قَانِتٗا لِّلَّهِ حَنِيفٗا وَلَمْ يَكُ مِنَ اَ۬لْمُشْرِكِينَ ﴿120﴾
شَاكِرٗا لِّأَنْعُمِهِۦٓ اِ۪جْتَبَٰلهُ وَهَدَٰلهُ إِلَيٰ صِرَٰطٖ مُّسْتَقِيمٖ ﴿121﴾
وَءَاتَيْنَٰهُ فِي اِ۬لدُّنْيَا حَسَنَةٗ وَإِنَّهُۥ فِي اِ۬لْأٓخِرَةِ لَمِنَ
اَ۬لصَّٰلِحِينَ ﴿122﴾ ثُمَّ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ أَنِ اِ۪تَّبِعْ مِلَّةَ إِبْرَٰهِيمَ
حَنِيفٗا وَمَا كَانَ مِنَ اَ۬لْمُشْرِكِينَ ﴿123﴾ إِنَّمَا جُعِلَ اَ۬لسَّبْتُ
عَلَى اَ۬لَّذِينَ اَ۪خْتَلَفُواْ فِيهِ وَإِنَّ رَبَّكَ لَيَحْكُمُ بَيْنَهُمْ يَوْمَ
اَ۬لْقِيَٰمَةِ فِيمَا كَانُواْ فِيهِ يَخْتَلِفُونَ ﴿124﴾ اُدْعُ إِلَيٰ سَبِيلِ
رَبِّكَ بِالْحِكْمَةِ وَالْمَوْعِظَةِ اِ۬لْحَسَنَةِ وَجَٰدِلْهُم بِالَّتِي
هِيَ أَحْسَنُ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعْلَمُ بِمَن ضَلَّ عَن سَبِيلِهِۦ
وَهُوَ أَعْلَمُ بِالْمُهْتَدِينَ ﴿125﴾ وَإِنْ عَاقَبْتُمْ فَعَاقِبُواْ بِمِثْلِ
مَا عُوقِبْتُم بِهِۦ وَلَئِن صَبَرْتُمْ لَهُوَ خَيْرٞ لِّلصَّٰبِرِينَ ﴿126﴾ وَاصْبِرْ
وَمَا صَبْرُكَ إِلَّا بِاللَّهِ وَلَا تَحْزَنْ عَلَيْهِمْ وَلَا تَكُ فِي ضَيْقٖ مِّمَّا يَمْكُرُونَ ﴿127﴾
إِنَّ اَ۬للَّهَ مَعَ اَ۬لَّذِينَ اَ۪تَّقَواْ وَّالَّذِينَ هُم مُّحْسِنُونَ ﴿128﴾

119. Sannan haƙiƙa Ubangijinka mai gafara ne mai jinƙai ga waɗanda suka aikata mummuna dajahilci sannan suka tuba bayan wancananka, sannan suka gyara aikinsu, haƙiƙa Ubangijinka bayan wannan (jahilci da tuba) mai gafara ne, mai jinƙai (a garesu.)

120. Haƙiƙa Annabi Ibrahim (mai tsiran Allah da amincinsa) limami ne mai ibada ga Ubangijinsa wanda yake kan addinin totar, bai kasance daga cikin mushirikai ba.

121. Mai tunawa da ni'imominsa ya zaɓe shiya shirye shi izuwa tafarki madaidaici.

122. Munbashi kyakkyawan ambato a duniya, haƙiƙa shi a lahira yana daga cikin sahihai (ma'abucin darajoji maɗaukaka.)

123. Sannan muka aiko zuwa gareka (Ya Annabi mai tsira da amincin Allah) izuwa gareka cewa ka bi addinin Annabi Ibrahim (mai tsira da amincin Allah) mai totar, bai kasance daga cikin mushirikai ba.

(WAJADCIN GIRMAMA JUMA'A DA SHAGALA DA IBADA A CIKINTA MAIMAKON ASABAR DA LAHADI)

124. Haƙiƙa an sanya Asabar ga waɗannan da sukayi sabani a cikinsa (sune Yahudu, an umarce su su wofinta a cikinsa saboda ibada ranar Juma'a, sukace basu yarda basuka zabi Asabar, sai aka tsananta a garesu a cikinsa) haƙiƙa Ubangijinka yana hukunci tsakaninsu ranar Alƙiyama a kan abinda suke sassaɓawa a cikinsa (yayi wa mai sabo azaba saboda keta alfarmar Asabar.)

(KIRA IZUWA ALLAH)

125. Yi kira (Ya Annabi mai tsira da amincin Allah) izuwa addinin Ubangijinka da hikima (alƙur'ani) da gargaɗi kyakkyawa, kayi jayayya dasu da jayayyar da tafi kyau, (kamar kiran su izuwa ALLAH da ayoyinsa da kira izuwa hujjojinsa,) haƙiƙa Ubangijinka shine masani da wanda ya bata ga buran hanyarsa shine masani dashiryayyu.(Yayin da aka kashe Jarmai Hamza, akayi masa caɓai Manzon Allah mai tsira da aminci yagan shi, sai yace; Wallahi zan yi caɓai da mutum saba'in nasu a maimakon ka sai aka saukar da-:)

(CIKAK KEN ADALCI YANA GA SHARIAR MUSULUMCI)

126. Idan zakuyi uƙubakuyi uƙubada misalin abinda akayi muku uƙubadashi, Wallahi in kuka daure ga buran azaba, haƙiƙa dauriyar nan Itace tafi ga masu haƙuri. (Sai Manzon Allah mai tsira da amincin Allah ya hanu ga buran sakayya yayi kaffara ga rantsuwarsa.)

127. Ka haƙura, haƙurin ka bai kasance ba saida gamdakatar ɗin Allah, kada kayi baƙin ciki a kan kafirai (idan basu bada gaskiya ba, saboda kwaɗayin ka a kan imaninsu,) kadaka kasance cikin ƙunci daga makircin dasuke yi (kadaka damu, mu masu taimakonka ne a kansu.)

128. Haƙiƙa Ubangiji yana tareda masu tsoran sa da masu kyautatawa (da biyayya a cikin matsayin IHSANI.)

17 سُورَةُ الإِسْرَآءِ مَكِّيَّةٌ
وَهِيَ مِائَةٌ وَعَشْرُ ءَايَاتٍ 110

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

حزب

* سُبْحَٰنَ الَّذِي أَسْرَىٰ بِعَبْدِهِ لَيْلًا مِّنَ الْمَسْجِدِ الْحَرَامِ إِلَى الْمَسْجِدِ
الْأَقْصَا الَّذِي بَٰرَكْنَا حَوْلَهُ لِنُرِيَهُ مِنْ ءَايَٰتِنَا إِنَّهُ هُوَ السَّمِيعُ
الْبَصِيرُ (1) وَءَاتَيْنَا مُوسَى الْكِتَٰبَ وَجَعَلْنَٰهُ هُدًى لِّبَنِي إِسْرَآءِيلَ
أَلَّا تَتَّخِذُوا مِن دُونِي وَكِيلًا (2) ذُرِّيَّةَ مَنْ حَمَلْنَا مَعَ نُوحٍ
إِنَّهُ كَانَ عَبْدًا شَكُورًا (3) وَقَضَيْنَا إِلَىٰ بَنِي إِسْرَآءِيلَ
فِي الْكِتَٰبِ لَتُفْسِدُنَّ فِي الْأَرْضِ مَرَّتَيْنِ وَلَتَعْلُنَّ عُلُوًّا كَبِيرًا (4)
فَإِذَا جَآءَ وَعْدُ أُولَىٰهُمَا بَعَثْنَا عَلَيْكُمْ عِبَادًا لَّنَا أُوْلِي بَأْسٍ شَدِيدٍ
فَجَاسُوا خِلَٰلَ الدِّيَارِ وَكَانَ وَعْدًا مَّفْعُولًا (5) ثُمَّ رَدَدْنَا لَكُمُ
الْكَرَّةَ عَلَيْهِمْ وَأَمْدَدْنَٰكُم بِأَمْوَٰلٍ وَبَنِينَ وَجَعَلْنَٰكُمْ
أَكْثَرَ نَفِيرًا (6) إِنْ أَحْسَنتُمْ أَحْسَنتُمْ لِأَنفُسِكُمْ وَإِنْ أَسَأْتُمْ فَلَهَا
فَإِذَا جَآءَ وَعْدُ الْأَخِرَةِ لِيَسُـءُوا وُجُوهَكُمْ وَلِيَدْخُلُوا الْمَسْجِدَ
كَمَا دَخَلُوهُ أَوَّلَ مَرَّةٍ وَلِيُتَبِّرُوا مَا عَلَوْا تَتْبِيرًا (7)

Suratul Isra'i

A Makka Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Dari Da Goma (110)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabaɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

(Ita wannan sura ana ambatonta Surar Bani-Isra'ila, ana ce da ita Surar Subhana, ta ƙunshi ma-ganganu a kan ƙudure-ƙudure na Musulunci da girman Man-zon Allah mai tsira da amincin Allah da aikensa da Alƙur'ani dashiriyar sa da matsayin mutane game da Alƙur'ani. Tayi zance ga mutum, da kyakkyawar hanyar sa da asalan matattara na Musulunci lafiyayye, da tsarkake Ubangiji ga buran abinda bai dace dashi ba, da labaran Bani-Isra'ila da Annabi Adamu mai tsira da amincin Allah. Ta fara magana a kan Isra'i, wato tafiyar dare wadda akayi da Annabi mai tsira da amincin Allah)

TAFIYAR DARE IZUWA GANAWA DA ALLAH (S.W.T.) DA GANIN MANA KAN SAMA

1. Tsarki ya tabbatarwa wanda yayi tafiyar dare da bawansa (Annabi mai tsira da amincin Allah) a dan yanki na dare, cikin mudda ƙanƙanuwa daga masallaci mai alfarma (Makka), izuwa masallaci mafi nisa (Baitul-Maƙadisi an ambace shi mafi nisa saboda nisan sa daga gareshi,) wanda mukayi albarka daura dashi (da Annabawa masu tsiran Allah da amincinsa da Waliyyai, Allah ya yarda dasu, da ƙoramu da "ya"yan itatuwa, don mu nuna masa mana -kan ikonmu, haƙiƙa (Manzon Allah mai tsiran Allah da amincinsa*) (1)
2. Mun baiwa Annabi Musa (Mai tsira da aminci) Attaura, Mun sanyashi shiriyaga Bani-Isra'ila don kadaku ,riƙi wani wakili bani ba.
3. Yaku zuriyar wanda muka ɗauke su a cikin jirgi tareda Annabi Nuhu, haƙiƙa shi Annabi Nuhu (mai tsira da amincin Allah) ya kasance mai yawan godiyaga Allah (a cikin dukkan haluluwansa).

(TACACCEN TARIHIN BANI-ISRA'ILA)

4. Mun aiko izuwa Bani-Isra'ila a cikin Attaura, lalle zakuyi ɓarna a cikin ƙasar (Sham, da saɓo) sau biyu, Wallahi zakuyi zalunci, zalunci mai girma.
5. Idan lokacin ɓarnar ta farkonsa tazo zamu sako bayi a kanku namu, ma'abota tsananin yaƙi, zasu kaikawo (saboda neman ku,) a tsatstsakin gidajen ku (donsu kashe ku su ribace ku) Wance -nanka sako bayin nan da bincikensu tsatstsakin gidajensu ya kasance alƙawari ne abin aikatawa. (Sun yi ɓarnar farko da kashe Annabi Zakariya'u mai tsiran Allah da aminci aka sako Jalutu a kansu da rundunarsa suka kashe su suka ribace "ya"yansu suka msa Baitul-Maƙadisi.)
6. Sannan muka mai da juyowa gareku a kansu, (bayan shekara ɗari da kashe Jalutu,) muka kare kuda dukiyoyi da "ya"yaye, muka sanya ku mafiya yawan dangi.

1) Hikimar Kamanta Annabi mai tsira da amincin Allah da waɗannan sunannaki guda biyu a wannan wurc, jurewarsa ganin Ubangigi da jin zanccnsa bakidaya, wacce ba tayiwu ga Annabi Musa mai tsira da Amincin Allah ba, duba sawii.

*shine mai cikakken ji da gani, Ko Ubangiji, saboda ganin sa mana kan ikon Allah da jin zancen Ubangiji da ganin Zatinsa, ko saboda Ubangiji shine mai jin maganganunsa da ayyukansa, dana waninsa mai ganinsu, Ubangiji yayi wa An-nabi mai tsira da amincin Allah cikakkiyar ni'ima da wannan tafiya ta dare dayayi dashi, saboda . a shine ya tarar da Annabawa masu tsiran Allah da amincinsa ya hau izuwa sammai da ganin mana kon zuzzurfan ikon Allah da ganawa dashi) saboda shi Manzon Allah mai tsira da amincin Allah yace, An zo min da Buraƙa, ita kuwa dabbace fara tafi jaki girma komabayan alfadari, tana ajiye kofa-tanta yadda matukar ganinta ya tuƙe, saina hau ta saita tafi dani har na je Baitul-Maƙadisi na ɗaure ta a wannan zobe wacce Annabawa masu tsiran Allah da amincinsa suke daurewa, sannan na shiga na sallaci raka'a biyu a cikinsa, sannan na fito, Mala'ika =

ثمن

عَسَىٰ رَبُّكُمْ أَنْ يَرْحَمَكُمْ وَإِنْ عُدتُّمْ عُدْنَا وَجَعَلْنَا جَهَنَّمَ
لِلْكَٰفِرِينَ حَصِيرًا ﴿8﴾ إِنَّ هَٰذَا الْقُرْءَانَ يَهْدِي لِلَّتِي هِيَ أَقْوَمُ وَيُبَشِّرُ
الْمُؤْمِنِينَ الَّذِينَ يَعْمَلُونَ الصَّٰلِحَٰتِ أَنَّ لَهُمْ أَجْرًا كَبِيرًا ﴿9﴾ وَأَنَّ الَّذِينَ
لَا يُؤْمِنُونَ بِالْءَاخِرَةِ أَعْتَدْنَا لَهُمْ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿10﴾ * وَيَدْعُ الْإِنسَٰنُ بِالشَّرِّ
دُعَآءَهُ بِالْخَيْرِ وَكَانَ الْإِنسَٰنُ عَجُولًا ﴿11﴾ وَجَعَلْنَا الَّيْلَ وَالنَّهَارَ ءَايَتَيْنِ
فَمَحَوْنَا ءَايَةَ الَّيْلِ وَجَعَلْنَا ءَايَةَ النَّهَارِ مُبْصِرَةً لِّتَبْتَغُوا فَضْلًا مِّن رَّبِّكُمْ
وَلِتَعْلَمُوا عَدَدَ السِّنِينَ وَالْحِسَابَ وَكُلَّ شَيْءٍ فَصَّلْنَٰهُ
تَفْصِيلًا ﴿12﴾ وَكُلَّ إِنسَٰنٍ أَلْزَمْنَٰهُ طَٰٓئِرَهُ فِي عُنُقِهِ وَنُخْرِجُ لَهُ
يَوْمَ الْقِيَٰمَةِ كِتَٰبًا يَلْقَىٰهُ مَنشُورًا ﴿13﴾ اقْرَأْ كِتَٰبَكَ كَفَىٰ
بِنَفْسِكَ الْيَوْمَ عَلَيْكَ حَسِيبًا ﴿14﴾ مَّنِ اهْتَدَىٰ فَإِنَّمَا يَهْتَدِي
لِنَفْسِهِ وَمَن ضَلَّ فَإِنَّمَا يَضِلُّ عَلَيْهَا وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٌ وِزْرَ أُخْرَىٰ
وَمَا كُنَّا مُعَذِّبِينَ حَتَّىٰ نَبْعَثَ رَسُولًا ﴿15﴾ وَإِذَا أَرَدْنَا
أَن نُّهْلِكَ قَرْيَةً أَمَرْنَا مُتْرَفِيهَا فَفَسَقُوا فِيهَا فَحَقَّ عَلَيْهَا الْقَوْلُ
فَدَمَّرْنَٰهَا تَدْمِيرًا ﴿16﴾ وَكَمْ أَهْلَكْنَا مِنَ الْقُرُونِ
مِنْ بَعْدِ نُوحٍ وَكَفَىٰ بِرَبِّكَ بِذُنُوبِ عِبَادِهِ خَبِيرًا بَصِيرًا ﴿17﴾

7. Mukace in kun kyautata (da ɗa'a) kun kyautata ga kawukan ku (domin sakamakon na kanku ne,) idan ku ka ɓata (da ɓarna,) to, ɓatawar nan gareku ce, to, idan alƙawarin marrar ƙarshe yazo, to, sai mu sako su donsu tursasa fuskokin ku (da kisa da ribacewa,) kuma saboda su shiga masallacin Baitul-Maƙadisi su risbashi tamfar da suka shige shi suka rusa shi marrar farko, don kuma su halakar da abinda sukayi rinjaye kansa halakarwa (sun yi ɓarna marrar ta biyu da kashe Annabi Yahaya mai tsiran Allah da amincinsa aka sako Buhtu-Nasar a kansu ya kashe dubbai daga garesu ya ribace zuriyyarsu, ya msa Baitul-Maƙadisi, muka faɗa a cikin Attaura-)
8. Ana kauna Ubangijinku yajiƙan ku bayan marra ta biyu in kun tuba, in kun koma (izuwa ɓarna,) ma koma (izuwa uƙuba, sun koma da ƙaryata Manzon Allah ne tsira da amincin Allah, sai aka salladashi a kansu, ya kashe kuraizatu yakore Narilu ya sa jizya a kansu.) Mun sanya jahannama tabarma ga kafirai, (wato kurkukunsu.)
9. Haƙiƙa wannan Alƙur'ani yana shiryarwa izuwa hanyar data ti daidai, yanayi wa muminai albishir waɗanda suke aikata ayyuka nagari cewa haƙiƙa lada mai girma yana garesu.
10. Haƙiƙa kuma yana bada labari cewa waɗanda basu bada gaskiya da lahira ba, mun tanaji azaba mai raɗaɗi garesu.
11. Mutum yana addu'a da sharri ga kansa ga iyalinsa idan ya sike, irin yadda yake addu'a da alheri, haƙiƙa mutum ya kasance mai garaje (da addu'a a kansa da rashin tunani a cikin ƙarshen al'amari.) (WANI ABU DAGA NI'IMOMIN ALLAH A GAREMU DA ILIMIN TAURARI DA LISSAFI)
12. Mun sanya dare da wuni aya guda biyu (masu nuna ikonmu,) muka shafe ayar dare, (wato muka tafi da haskenta, don saboda su nutsu a cikinsa,) muka sanya ayar wuni mai ganar dasu (abin gani a cikinta saboda haske) don ku nemi falala daga Ubangijnku (da tsuwurwuri,) kuma don ku san adadin shekaru da lissafin lokatai. Mun rarraba kowane abu (da ake bukata gareshi) rarrabewa.
13. Kowane mutum mun lazumta masa aikinsa zai dauke shi a kan wuyansa, (Mujahidu yace babu wani abin haihuwa daza a haife shi face akwai takarda a cikin wuyansa, an rubuta a cikinta shaƙiyyi ne ko sadauki ne) zamu fitar masa littafinsa abin rubutawar aikinsa a ciki, kuma zai hadu dashi abin ɗaiɗaitawa.
14. Za a ce dashi karanta littafin ka, kanka ta isa mai lissafi a kanka a wannan rana.

(HANZARIN MUTAN FATARA DA WANDA KIRA BAI ZO MUSU BA)

15. Wanda ya shiriya, ya shiriya don kansa, domin sakamakon shiriyar nan na ga kansa, ba wata kai mai zunubi da zata dauki zunubin wata kai. Bamu kasance masu azaba ga kowa ba sai mun aiko jakada.
16. Idan mun nufi zamu halakar da mutanen alƙarya, to, sai mu umarci shiyagabannin tada bin Ubangiji a bisa harshen manzanninmu sai suyi fasikanci a cikinta, sai magana ta tabbata a garemu dayi musu azaba, sai mu halakar da ita, halakarwa.
17. Da yawa muka halakar daga tsareku, bayan Annabi Nuhu mai tsiran Allah da amincinsa. Ubangijinka ya isa masanin zahirin al'amari da badinin sa, mai ganin komai da komai. (MAI NUFIN DUNIYA DA MAI NUFIN LAHIRA)

= Jibrilu mai tsira da amincin Allah yazo min da ƙwarya ta giya da ƙwarya ta nono, saina zaɓi nonon, sai Jibrilu mai tsira da amincin Allah yace, Ka dace dasunna sannan aka hau dani izuwa sama ta duniya, Mala'ika Jibrilu mai tsira da amincin Allah yace a buɗe, akace waye kai? Yace Jibrilu ne, akace waye tareda kai? Yace Muhammadu mai tsira da amincin Allah, akace an aika masa ne? Yace an aika masa, aka buɗe mana, sai ga ni da An-nabi Adamu mai tsira da amincin Allah, yayi marabadani yayi min addu'a da alheri, sannan aka hau dani izuwa sama ta biyu, Mala'ika Jibrilu ya nemi a buɗe, akace waye kai? Yace Jibrilu, akace waye tareda kai? Yace Muhammadu mai tsira da amincin Allah, akace an aiko izuwa gareshi? Yace an aika. izuwa gareshi, sai aka buɗe mana, sai ga ni da "ya"ya biyu na Yakumbo wato "ya"ya biyu na "yar uwar uwa, Annabi Yahaya da Annabi Isa, sukayi marabadani sukayi min addu'a da alheri, sannan aka hau dani izuwa sama ta uku, Mala'ika Jibrilu yace a buɗe, akace waye? =

مَن كَانَ يُرِيدُ الْعَاجِلَةَ عَجَّلْنَا لَهُۥ فِيهَا مَا نَشَآءُ لِمَن نُّرِيدُ
ثُمَّ جَعَلْنَا لَهُۥ جَهَنَّمَ يَصْلَيٰهَا مَذْمُوماً مَّدْحُوراً ﴿18﴾ وَمَنْ أَرَادَ
ءَالَاخِرَةَ وَسَعَيٰ لَهَا سَعْيَهَا وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَأُوْلَٰٓئِكَ كَانَ سَعْيُهُم
مَّشْكُوراً ﴿19﴾ كُلّاً نُّمِدُّ هَٰٓؤُلَآءِ وَهَٰٓؤُلَآءِ مِنْ عَطَآءِ رَبِّكَ
وَمَا كَانَ عَطَآءُ رَبِّكَ مَحْظُوراً ﴿20﴾ انظُرْ كَيْفَ فَضَّلْنَا بَعْضَهُمْ
عَلَيٰ بَعْضٍ وَلَلَاخِرَةُ أَكْبَرُ دَرَجَٰتٍ وَأَكْبَرُ تَفْضِيلاً ﴿21﴾
لَّا تَجْعَلْ مَعَ اللَّهِ إِلَٰهاً ءَاخَرَ فَتَقْعُدَ مَذْمُوماً مَّخْذُولاً ﴿22﴾
* وَقَضَيٰ رَبُّكَ أَلَّا تَعْبُدُوٓاْ إِلَّآ إِيَّاهُ وَبِالْوَٰلِدَيْنِ إِحْسَٰناً
إِمَّا يَبْلُغَنَّ عِندَكَ الْكِبَرَ أَحَدُهُمَآ أَوْ كِلَاهُمَا فَلَا تَقُل لَّهُمَآ
أُفٍّ وَلَا تَنْهَرْهُمَا وَقُل لَّهُمَا قَوْلاً كَرِيماً ﴿23﴾ وَاخْفِضْ لَهُمَا جَنَاحَ
الذُّلِّ مِنَ الرَّحْمَةِ وَقُل رَّبِّ ارْحَمْهُمَا كَمَا رَبَّيَٰنِيَ صَغِيراً ﴿24﴾
رَّبُّكُمْ أَعْلَمُ بِمَا فِي نُفُوسِكُمْ إِن تَكُونُواْ صَٰلِحِينَ فَإِنَّهُۥ كَانَ
لِلْأَوَّٰبِينَ غَفُوراً ﴿25﴾ وَءَاتِ ذَا الْقُرْبَيٰ حَقَّهُۥ وَالْمِسْكِينَ
وَابْنَ السَّبِيلِ وَلَا تُبَذِّرْ تَبْذِيراً ﴿26﴾ إِنَّ الْمُبَذِّرِينَ كَانُوٓاْ
إِخْوَٰنَ الشَّيَٰطِينِ وَكَانَ الشَّيْطَٰنُ لِرَبِّهِۦ كَفُوراً ﴿27﴾

رُبُع

18. Wanda ya kasance yana nufin duniya (da aikinsa,) sai mu gaggauta abinda muka ga dama ga wanda muka ga dama (gareshi) a cikinta, sannan mu sanya jahannama gareshi a lahira ya shige ta abin zargi a bin korewa (ga buran rahamar Allah, Allah ya kiyashe mu amin.)
19. Wanda yake nufin lahira da aikinsa, yayi ƙoƙari ya aikata aiki irin nata a garc ta alhali shi yana mai bada gaskiya da Ubangiji, To, waɗancananka aikinsu ya kasance abin godewa (nan ga Allah).
20. Kowane ɗaya (daga jama'ar nan guda biyu) muna ƙarinsu waɗannan da waɗannan, daga baiwar Ubangijinka (a duniya), haƙiƙa baiwar Ubangijinka bata kasance abar hanawa ba (ga kowa).
21. Ka duba ƙaƙa muka fifita ba'alinsu a kan ba'ali (a cikin arziki da alfarma,) to, haƙiƙa lahira Itace tafi girman darajoji, tafi yawan fifitawa (daga duniya, ya kamata a kula da ita matuka).

(AL'AMUDAN MUSULUNCI NA RAYUWA CIKIN JAMA'A, TSARKAKE AIKI WATO IHLASI DA SAKAMAKON RASHIN YINSA)

22. Kadaka sanya wani ubangiji dabam tareda Allah, bare ka zama abin zargi abin tabarwa.
23. Ubangijinka ya hukunta kadaku ,bautawa kowa sai shi.

(BIN IYAYE)

Ubangiji yayi umarni da kyautata wa iyaye kyautatawa, idan ɗayansu ya isa girma nan gareka, ko dukkansu su biyu, to, kada kace dasu affafairan, kada kuma kayi musu tsawa, ka gaya musu magana mai girma mai taushi.

24. Ka tausasa musu janubinka mai taushi horarre don jinƙai garesu, ka ce, "Ubangiji! kaji ƙansu. tamfar da suka jiƙaina, lokacin da suka rene ni ina dan ƙanƙane".
25. Ubangijinkune masani da abinda yake cikin zukatanku (nadaga biyayyako fitsara,) in kun kasance managarta, to haƙiƙa Ubangiji mai gafara ne ga masu komawa izuwa bin Ubangiji, zai gafarta musu abinda ya auku daga garesu da kuskure, wato abinda sukayi wa iyaye bada niyya ba.

(SADAR DA ZUMUNTA)

26. Ka baiwa ma'abucin zumunci haƙƙinsa (nadaga biyayya da sada zumunta) da miskini (wato mabukaci,) da dan hanya: (HANI GA AL MUBAZ ZARANCI) (Kada kayi almubazzaranci (wato ka ciyar ba cikin bin Allah ba, ba almubazzaranci ga wandazai ciyar saboda Allah).
27. Haƙiƙa masu almubazzaranci sun kasance yan uwan sheɗanu (wato hanyarsu) shi ko sheɗan ya kasance mai tsananin kafircewa da ni'imar ubangijinsa.

= Yace Jibrilu, akace waye tareda kai? Yace Muhammadu ne mai tsiran Allah da amincinsa, akace an tura masa jakada ne, yace an tura masa, sai aka buɗe mana, sai ga ni da Annabi Yusufu, sai gashi an bashi rabin kyau, yayi marabadani yayi min addu'a da alheri, sannan aka hau da mu izuwa sama ta hudu, Jibrilu ya nemi a buɗe, akace waye, yace Jibrilu, akace waye tareda kai, yace Muhammadu mai tsiran Allah da amincinsa, akace an tura masa jakada ne? Yace an aika izuwa gareshi, sai aka buɗe mana, sai ga ni da Annabi Idrisu, yayi marabadani yayi min addu'a da alheri, sannan aka hau dani izuwa sama ta biyar Mala'ika Jibrilu ya nemi a bude, akace waye, yace Jibrilu, akace waye tareda kai, yace Muhammadu ne mai tsira da amincin Allah, akace an aika izuwa gareshi? Yace an aika izuwa gareshi, sai aka bude mana, sai ga ni da Annabi Haruna, yayi marabadani yayi min addu'a da alheri, sannan aka hau dani izuwa sama ta shida, Mala'ika Jibrilu ya nemi a buɗe, akace waye, yace Jibrilu, akace waye tareda kai? Yace Muhammadu mai tsira da amincin Allah, akace an aika izuwa gareshine? yace an aika izuwa gareshi, sai aka buɗe mana, sai ga ni da Annabi Musa, yayi marabadani yayi min addu'a da alheri, sannan aka hau da mu izuwa sama ta bakwai, Jibrilu, ya nemi a buɗe, akace waye, yace Jibrilu, akace waye taredakai yace Muhammadu mai tsira da amincin Allah, akace an aika izuwa gareshine yace an aika izuwa gareshi, sai aka buɗe mana sai ga ni da Annabi Ibrahim, sai gashiya jingina izuwa Baitul-Ma'amuru, sai gashi Mala'ika dubu saba'in yana shigarsa a kowace rana, sannan bazasu komo izuwa gareshi ba, sannan aka tafi dani =

وَإِمَّا تُعْرِضَنَّ عَنْهُمُ اُ۪بْتِغَآءَ رَحْمَةٖ مِّن رَّبِّكَ تَرْجُوهَا فَقُل لَّهُمْ
قَوْلاٗ مَّيْسُوراٗ ﴿28﴾ وَلَا تَجْعَلْ يَدَكَ مَغْلُولَةً اِلَيٰ عُنُقِكَ وَلَا تَبْسُطْهَا
كُلَّ اَ۬لْبَسْطِ فَتَقْعُدَ مَلُوماٗ مَّحْسُوراً ﴿29﴾ اِنَّ رَبَّكَ يَبْسُطُ اُ۬لرِّزْقَ
لِمَنْ يَّشَآءُ وَيَقْدِرُۥٓ إِنَّهُۥ كَانَ بِعِبَادِهِۦ خَبِيراَۢ بَصِيراٗ ﴿30﴾ وَلَا تَقْتُلُوٓاْ
أَوْلَٰدَكُمْ خَشْيَةَ إِمْلَٰقٖ نَّحْنُ نَرْزُقُهُمْ وَإِيَّاكُمُۥٓ إِنَّ قَتْلَهُمْ
كَانَ خِطْـٔاٗ كَبِيراٗ ﴿31﴾ وَلَا تَقْرَبُواْ اُ۬لزِّنَيٰٓ إِنَّهُۥ كَانَ فَٰحِشَةٗ وَسَآءَ
سَبِيلاٗ ﴿32﴾ وَلَا تَقْتُلُواْ اُ۬لنَّفْسَ اَ۬لتِے حَرَّمَ اَ۬للَّهُ إِلَّا بِالْحَقِّ
وَمَن قُتِلَ مَظْلُوماٗ فَقَدْ جَعَلْنَا لِوَلِيِّهِۦ سُلْطَٰناٗ فَلَا يُسْرِف فِّے اِ۬لْقَتْلِ
إِنَّهُۥ كَانَ مَنصُوراٗ ﴿33﴾ وَلَا تَقْرَبُواْ مَالَ اَ۬لْيَتِيمِ إِلَّا بِالتِے هِيَ أَحْسَنُ
حَتَّيٰ يَبْلُغَ أَشُدَّهُۥ وَأَوْفُواْ بِالْعَهْدِ إِنَّ اَ۬لْعَهْدَ كَانَ مَسْـُٔولاٗ ﴿34﴾
وَأَوْفُواْ اُ۬لْكَيْلَ إِذَا كِلْتُمْ وَزِنُواْ بِالْقُسْطَاسِ اِ۬لْمُسْتَقِيمِ
ذَٰلِكَ خَيْرٞ وَأَحْسَنُ تَأْوِيلاٗ ﴿35﴾ * وَلَا تَقْفُ مَا لَيْسَ لَكَ بِهِۦ عِلْمٌ
إِنَّ اَ۬لسَّمْعَ وَالْبَصَرَ وَالْفُؤَادَ كُلُّ أُوْلَٰٓئِكَ كَانَ عَنْهُ مَسْـُٔولاٗ ﴿36﴾
وَلَا تَمْشِ فِے اِ۬لْأَرْضِ مَرَحاً اِنَّكَ لَن تَخْرِقَ اَ۬لْأَرْضَ وَلَن تَبْلُغَ اَ۬لْجِبَالَ
طُولاٗ ﴿37﴾ كُلُّ ذَٰلِكَ كَانَ سَيِّئَةً عِندَ رَبِّكَ مَكْرُوهاٗ ﴿38﴾

ثمن

28. To, in ka bujire ga buransu, su yan uwanka, (baka basu komai ba) saboda sauraron rahama daga Ubangijinka (wato arziki da kake sauraron yazo maka ka basu,) to gaya musu magana mai sauki (wato kayi musu alƙawari da bayarwa in Allah ya baka.)

29. Kadaka sanya hannunka abin kukuncewa izuwa wuyanka, (wato kadaka rike ta cikin ciyarwa matukar riƙewa,) kadaka saketa cikin ciyarwa dukkan saki, bare ka zauna abin zargi yankakke, banbar.

30. Haƙiƙa Ubangijinka yana yalwata arziki ga wanda yaga dama yana kuntatawa ga wanda yaga dama, haƙiƙa Ubangiji ya kasance masanin badinin bayinsa da zahirinsu (zai azurta su da gwargwadon masalaharsu).

(HANI GA BURAN BINNEWAR 'YA'YADARAI)

31. Kadaku ,kashe 'ya'yanku (wato kadaku ,binne su da rai) don tsoron talauci, Mune masu azurta ku masu azurta su, kashe su ya kasance zunubi maigirma.

(HANI GA ZINA DA KISAN KAI)

32. Kadaku ,kusanci zina haƙiƙa ita zina ta kasance mummuna ta munana tafarki.

33. Kadaku ,kashe kai wacce Allah ya haramta saida gaskiya, wanda aka kashe shi abin zalunta haƙiƙa mun sanya bin jini ga waliyyinsa, (wato magajinsa) to kada yayi shishshig. a cikin kisa (wato ya kashe wanin wanda ya kashe shi ko kuma a kashe shi bada abinda yayi kisa dashi ba, muddin bada haram yayi kisa bakamar zina ko waninta, in haka ta faru sai a kashe shi da kansakali.) Haƙiƙa shiya kasance abin taimako.

(HANI GA DUKIYAR MARAYA DA CIKA MUDU)

34. Kadaku ,kusanci dukiyar maraya, saida hali wacce take mafi kyau, har ya isa ganiyarsa, ku cika da alƙawari in kun yi wa (Allah ko mutane,) haƙiƙa alƙawari ya kasance abin tambayo gareshi.

35. Ku cika ma'auni idan zakuyi awo, ku auna da mudu madai-daici, wancananka shi yafi alheri yafi kyakkyawar makoma.

(HANI GA BARIN GAGGAWAR PATAWA DA TAKA TSANTSAN A CIKINTADA KAME JI DA GANI DA ZUCIYAGA BARIN ABINDA BAI KAMATA BA)

36. Kadaka bibiyi abinda baka da sani dashi haƙiƙa ji da gani da zuciya duk wadannan Allah zai tambayi mai su, me ya aikata dasu.

(UMARNI DA TAWALFU DA SAUKIN KAI)

37. Kada kayi tafiya a bayan ƙasa kana mai girman kai, haƙiƙa kai bazaka huda ƙasa har ka kai ƙarshentada girman kan ka ba, bazaka kai ga duwarwatsu a tsawo ba (saboda me za kayi taƙama).

38. Dukkan wannan abin ambato mummunansa abin ki ne a wa-jen Ubangijinka.

= izuwa magaryar tukewa, sai ga ganyayyakinta kamar kunnen giwa, sai ga "ya"yan itaciyarta kamar randuna, yayin da abinda masarautar Allah ya lulluɓe ta saita sauya kama, babu daya daga halittar dazai iya sifanta ta saboda kyanta, yacc Sai Ubangiji ya aiko min abinda ya aiko izuwa gare ni, ya wajabta min salla hamsin a cikin kowane wuni da dare har na tuke izuwa Annabi Musa, yace, Me Ubangijinka ya wajabta bisa al'umma, na ce salla hamsin a kowane wuni da dare, yace koma izuwa Ubangijinka ka roƙi rangwame, haƙiƙa al'ummarka bazata iya wannan ba, yace ni, haƙiƙa na jarrabi Bani-Isra'ila na san su, sai yace saina koma izuwa Ubangijina, na ce ya Ubangiji sauwaƙe ga al'umma ta, saiya sauwaƙe biyar, saina koma izuwa Anna-bi Musa yace, Me ka aikata, na ce; ya saryar min da salla biyar, yace,; al'ummar ka bazata iya wannan ba, koma izuwa Uban -gijinka ka roƙe shi rangwame, yace; ban gushe ba ina komawa tsakanin. Ubangijina da Annabi Musa yana rage min biyar-biyar har yace, Ya Muhammadu mai tsira da amincin Allah, su salloli ne guda biyar, a cikin kowane wuni da dare, kowace salla tana da lada goma in an hade. salla hamsin ke nan. Wanda yayi nufi da aikin alheri bai aikata baza a rubuta himmar nan tasa kyakkyawan aiki gareshi, idan =

ذَٰلِكَ مِمَّا أَوْحَىٰ إِلَيْكَ رَبُّكَ مِنَ الْحِكْمَةِ وَلَا تَجْعَلْ مَعَ اللَّهِ
إِلَٰهًا آخَرَ فَتُلْقَىٰ فِي جَهَنَّمَ مَلُومًا مَدْحُورًا ﴿39﴾ أَفَأَصْفَاكُمْ رَبُّكُم
بِالْبَنِينَ وَاتَّخَذَ مِنَ الْمَلَائِكَةِ إِنَاثًا إِنَّكُمْ لَتَقُولُونَ قَوْلًا عَظِيمًا ﴿40﴾
وَلَقَدْ صَرَّفْنَا فِي هَٰذَا الْقُرْءَانِ لِيَذَّكَّرُوا وَمَا يَزِيدُهُمْ
إِلَّا نُفُورًا ﴿41﴾ قُل لَّوْ كَانَ مَعَهُ ءَالِهَةٌ كَمَا تَقُولُونَ إِذًا لَّابْتَغَوْا
إِلَىٰ ذِي الْعَرْشِ سَبِيلًا ﴿42﴾ سُبْحَانَهُ وَتَعَالَىٰ عَمَّا يَقُولُونَ عُلُوًّا كَبِيرًا ﴿43﴾
يُسَبِّحُ لَهُ السَّمَاوَاتُ السَّبْعُ وَالْأَرْضُ وَمَن فِيهِنَّ وَإِن مِّن شَيْءٍ إِلَّا يُسَبِّحُ
بِحَمْدِهِ وَلَٰكِن لَّا تَفْقَهُونَ تَسْبِيحَهُمْ إِنَّهُ كَانَ حَلِيمًا غَفُورًا ﴿44﴾ وَإِذَا قَرَأْتَ
الْقُرْءَانَ جَعَلْنَا بَيْنَكَ وَبَيْنَ الَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِالْآخِرَةِ حِجَابًا مَّسْتُورًا ﴿45﴾
وَجَعَلْنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ أَكِنَّةً أَن يَفْقَهُوهُ وَفِي ءَاذَانِهِمْ وَقْرًا
وَإِذَا ذَكَرْتَ رَبَّكَ فِي الْقُرْءَانِ وَحْدَهُ وَلَّوْا عَلَىٰ أَدْبَارِهِمْ نُفُورًا ﴿46﴾
نَّحْنُ أَعْلَمُ بِمَا يَسْتَمِعُونَ بِهِ إِذْ يَسْتَمِعُونَ إِلَيْكَ وَإِذْ هُمْ نَجْوَىٰ
إِذْ يَقُولُ الظَّالِمُونَ إِن تَتَّبِعُونَ إِلَّا رَجُلًا مَّسْحُورًا ﴿47﴾ انظُرْ
كَيْفَ ضَرَبُوا لَكَ الْأَمْثَالَ فَضَلُّوا فَلَا يَسْتَطِيعُونَ سَبِيلًا ﴿48﴾ وَقَالُوا
أَءِذَا كُنَّا عِظَامًا وَرُفَاتًا أَءِنَّا لَمَبْعُوثُونَ خَلْقًا جَدِيدًا ﴿49﴾

39. Wancananka yana daga cikin abinda Ubangijinka ya aiko izuwa gareka na daga hikima, kadaka sanya wani Ubangiji daban abin bautawa tareda Allah, sai a jefa ka a cikin Jahannama kana abin zargi korarre daga rahamar Allah.

(TSARKAKE UBANGIJI DAGA ABINDA BAI KAMATA BA) DA SAKAMA KONSA

40. Yaya Ubangijinku zai keɓance kuda "ya"ya maza ya zabi Mala'iku "ya"yaye mata ga kansa a riyawarku, haƙiƙa ku kuna faɗin magana ne mai girma.

41. Lalle Mun bayyana a cikin wannan Alƙur'ani na misalce-misalce da wa'adi da wa'idi dan su gargaɗu, wannan bai ƙara musu komai ba sai gudu ga barin gaskiya.

(RADDI BISA WANDA YAYI DA'AWAR ABOKIN TARAYYA DA ALLAH)

42. Cenc dasu da iyayen giji sun kasance tareda Allah tamfar da kuke faɗa to, dasun nemi hanya izuwa Mahaliccin Al'arshi saboda su yake shi.

43. Tsarki ya tabbatar masa ya girma ga barin abinda suke faɗa na sharikai; ɗaukaka mai girma.

(TASBIHIN SAMMAI DA ƘASSAIDA MAKAMANTANSU WANDA AHLULLAHI SUKE CEWA DASHI ZIKIRULKAUNI DUK KAN KASANTATTU AMBATON ALLAH SUKE DA HARSHEN MAGANA DA HAR SHEN HALI)

44. Sammai bakwai da ƙassai suna ambaton Ubangiji da abinda yake cikinsu, babu wani abu daga ababan halittar Ubangiji face yana ambaton Allah, yana haɗawa da godiyarsa; yana cewa SubhanAllahi Wa biham-dihi, (Hadisan Annabi sun zoda tasbihin tsakwankwani da abinci da duwatsu da zancen raƙumi da damo da kura da barewa da dakalin ƙofa da sauransu) sai dai ba kwa fahimtar yadda zikirin nasa yake saboda cewa ba a cikin harshenku yake ba, (ko kuma toshiya da take cikin kun-nuwanku, amma akwai daga Ahlullahi wadanda suke fahimtar ZikirulKaum a cikin kowane harshe ya afku kamar Annabi Sulaimanu da babansa Annabi Dawuriu da sauran su [1] Haƙiƙa Ubangiji ya tabbata mai jinkirin azaba ga wanda ya cancanceta, mai yawan gafara gareshi saboda bai gaggauta uƙuba a gareku ba.

(KIYAYE MA'AIKIN ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA DA AMBATON WANDA ALLAH BAI NUFI ALHAIRI DASHI BA, KAMAR WANDA YA NIFI ZAIYI WA ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA KISAN GILA)

45. Idan kana karatun Ƙur'ani sai Mu sanya shamaki mai suturcewa tsakaninka da wanda bai bada gaskiya da ranar Lahira ba, bazasu ganka ba.

46. Muna sanya rufemfe a kan zu-katansu bazasu fahinci Al Ƙur'ani bamu kan sanya tashiya a cikin kunnuwansu baza suji shi jin Ƙarba ba. Idan ka ambaci Ubangijinka a AlƘur'ani Shi kaɗai saisu girka aguje don guje masa.

47. Mune masana da abinda suke sauraro saboda shi na izgili , yayin dasuke sauraro zuwa karatunka suna masu ganawa lokacin da azzalimai suke faɗa a cikin ganawarsu, ba kwa bin komai sai mutum abin rinjaye kan hankalinsa.

48. Kayi duba yaya suka buga mis-alce-misalce a gareka, sunce dakai boka, mawaki, marar hankali, suka ɓacewa gaskiya saboda wannan basu samun hanya izuwa ga wannan gaskiyar.

49. Suka faɗa suna musun tashin alƙyama, Yanzu in mun kasance kasusuwa rududdugaggii haƙiƙa mu za a tashe mu sabuwar halitta?

1) wannan fassara ta kasance bisa harshen haƙiƙa don kuwa shine haƙiƙa ı da aya ta kunsa. - Sanajıy –
= ko ya aikata ta za a rubuta masa lada goma, wanda yayi nufi da mugun aiki bai cika aikata ta ba, baza a rubuta komai ba, in ya aikata ta za a rubuta mummuna guda ɗaya, to, saina sauko har na tuke izuwa Annabi Musa na bashi labari, sai yace koma izuwa Ubangijinka ka roƙe shi rangwame, haƙiƙa al'umar ka bazata iya wannan ba, na ce haƙiƙa na koma izuwa Ubangijina har naji kunya -Buhari da Muslim sun ruwa ito wannan Hadisi) (amma lafizi na Musulum ne, Hakimu ya ruwa ito a cikin Mustadaraku ga Ibn Abbas yace, Ma'aikin Allah yace, na ga Ubangijina Mai girma da ɗaukaka.) (To jama'a wadannan hadisai sun kururutada cewa Annabi yaga Ubangiji Karara bada tawili ba, ya kamata sabani a kan ganin Allah game da Manzon Allah a =

ربع

۞ قُلْ كُونُواْ حِجَارَةً أَوْ حَدِيداً ﴿50﴾ أَوْ خَلْقاً مِّمَّا يَكْبُرُ فِي صُدُورِكُمْ
فَسَيَقُولُونَ مَنْ يُّعِيدُنَا قُلِ الذِے فَطَرَكُمُۥ أَوَّلَ مَرَّةٍ فَسَيُنْغِضُونَ
إِلَيْكَ رُءُوسَهُمْ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هُوَ قُلْ عَسَىٰ أَنْ يَّكُونَ قَرِيباً ﴿51﴾
يَوْمَ يَدْعُوكُمْ فَتَسْتَجِيبُونَ بِحَمْدِهِۦ وَتَظُنُّونَ إِن لَّبِثْتُمْ
إِلَّا قَلِيلاً ﴿52﴾ وَقُل لِّعِبَادِے يَقُولُواْ الَّتِے هِيَ أَحْسَنُ
إِنَّ الشَّيْطَٰنَ يَنزَغُ بَيْنَهُمْ إِنَّ الشَّيْطَٰنَ كَانَ لِلْإِنسَٰنِ عَدُوّاً
مُّبِيناً ﴿53﴾ رَّبُّكُمُۥ أَعْلَمُ بِكُمْ إِن يَّشَأْ يَرْحَمْكُمْ أَوْ إِن يَّشَأْ يُعَذِّبْكُمْ
وَمَا أَرْسَلْنَٰكَ عَلَيْهِمْ وَكِيلاً ﴿54﴾ وَرَبُّكَ أَعْلَمُ بِمَن فِي السَّمَٰوَٰتِ
وَالْأَرْضِ وَلَقَدْ فَضَّلْنَا بَعْضَ النَّبِيٓـِٕينَ عَلَىٰ بَعْضٍ وَءَاتَيْنَا دَاوُدَ
زَبُوراً ﴿55﴾ قُلُ ادْعُواْ الذِينَ زَعَمْتُم مِّن دُونِهِۦ فَلَا يَمْلِكُونَ
كَشْفَ الضُّرِّ عَنكُمْ وَلَا تَحْوِيلاً ﴿56﴾ أُوْلَٰٓئِكَ الذِينَ يَدْعُونَ
يَبْتَغُونَ إِلَىٰ رَبِّهِمُ الْوَسِيلَةَ أَيُّهُمُۥ أَقْرَبُ وَيَرْجُونَ رَحْمَتَهُۥ
وَيَخَافُونَ عَذَابَهُۥ إِنَّ عَذَابَ رَبِّكَ كَانَ مَحْذُوراً ﴿57﴾
وَإِن مِّن قَرْيَةٍ اِلَّا نَحْنُ مُهْلِكُوهَا قَبْلَ يَوْمِ الْقِيَٰمَةِ
أَوْ مُعَذِّبُوهَا عَذَاباً شَدِيداً كَانَ ذَٰلِكَ فِي الْكِتَٰبِ مَسْطُوراً ﴿58﴾

50. Cene dasu ku zamo duwarwatsu ko baƙin karfe.
51. Ko wata halitta daga abinda yake da girma a cikin zukatanku, a kan ya karɓi rayuwa, to, lalle sai an raYaku, da sannu zasu ce waye mai mayar da mu izuwa rayuwa? Cene wanda ya halicce ku a marar farko bakuna komai ba. To, da sannu zasu girgiza kansu izuwa gareka don mana ki, zasu ce don izgili yaushe ne wannan tashi? Cene Yakusanta ya zama a kusa.
52. Ranar da yake kiranku daga ƙaburbura a bisa harshen Israfila; ku amsa kiranSa daga ƙaburbura tareda godiyarSa, kuna zaton baku zauna a duniyaba sai kaɗan saboda tsoran abinda kuka gain

(KYAUTATAWA A CIKIN KIRA IZUWA ALLAH)

53. Ka faɗi ga bayi NA muminai su faɗa wa kafirai kalma wacce take kyakkyawa, haƙiƙa sheɗan yana ɓarna a tsakaninsu, kuma haƙiƙa sheɗan ya kasance mabayyanin ƙiyayyaga mutum. Kyakkyawar kalmar nan kuwa Itace;
54. Ubangijinkune mafi sani da ku, in yaga dama yajikankuda tubada imani, ko in yaga damar yi muku azaba yayi muku azabada mutuwa a kan kafirci, Bamu aikoka wakili a kansu ba bare ka tilashe su a kan imani, (wannan gaban umarni dayaƙi ne.)

(FIFITA MANZON ALLAH BISA ANNABAWA DA DARAJAR ISRA'I)

55. Ubangijinka nemasani da wanda yake cikin sammai da ƙassai, ya keɓance su da abinda yaga dama bisa gwargwadon haluluwansu. (Haƙiƙa Mun fifita sashin Annabawa a kan sashi da kebantar kowane daya daga garesu da fifiko, Annabi Musa da zance, Annabi Ibrahim da Badadantaka, Annabi Muhammadu da Tafiyar dare. Mun baiwa Annabi Dawuda Zabura).

MUNA KASHAR KAFIRAI CIKIN KUDURE - KUDURENSU

56. Cene (dasu) ku kira wadanda kuka riyacewa su iyayen giji ne ba Allah (kamar Mala'ikuda Annabi Isa da Uzairu) basu mallaki yaye cuta ga buranku ba, wala juya ta (izuwa waninku).
57. Waɗancananka waɗanda suke kiran (iyayen giji) suna neman saduwa ne izuwa ubangijinsu, wannenansune mafi kusanci izuwa gareshi. Suna kaunar rahamar Ubangiji suna tsoron azabarsa, haƙiƙa azabar Ubangijinka ta kasance abar tsoro.
58. Babu daga wata alɗarya (wato mutanenta) face mu, masu halakar da ita ne kafin ranar alƙiyama ko mu yi mata azaba, azaba mai tsanani (kisa da wa-ninsa,) Wancananka ya kasance abin rubutawa (a cikin Lauhul-Mahfuzu.)

= janye shi don waɗannan Hadisai guda Uku sun isa su zama Nassi yankakke a kan ganin Allah, wanda "AlRali lyal" yake cewa idan an sami Nassi = yankakke to ya wajaba a koma gareshi. wane yankakke ne yafi abinda buhari, da muslim da mustadraku suka ruwaito. Allah ne ma sani, Allah yayi mana mawafuka Amin. – Sanajiy)

وَمَا مَنَعَنَا أَن نُّرْسِلَ بِالْآيَاتِ إِلَّا أَن كَذَّبَ بِهَا الْأَوَّلُونَ
وَءَاتَيْنَا ثَمُودَ النَّاقَةَ مُبْصِرَةً فَظَلَمُوا بِهَا وَمَا نُرْسِلُ بِالْآيَاتِ
إِلَّا تَخْوِيفًا ﴿59﴾ وَإِذْ قُلْنَا لَكَ إِنَّ رَبَّكَ أَحَاطَ بِالنَّاسِ
وَمَا جَعَلْنَا الرُّءْيَا الَّتِي أَرَيْنَاكَ إِلَّا فِتْنَةً لِّلنَّاسِ
وَالشَّجَرَةَ الْمَلْعُونَةَ فِي الْقُرْءَانِ وَنُخَوِّفُهُمْ فَمَا يَزِيدُهُمْ
إِلَّا طُغْيَانًا كَبِيرًا ﴿60﴾ * وَإِذْ قُلْنَا لِلْمَلَائِكَةِ اسْجُدُوا لِآدَمَ
فَسَجَدُوا إِلَّا إِبْلِيسَ قَالَ ءَاسْجُدُ لِمَنْ خَلَقْتَ طِينًا ﴿61﴾
قَالَ أَرَأَيْتَكَ هَٰذَا الَّذِي كَرَّمْتَ عَلَيَّ لَئِنْ أَخَّرْتَنِي إِلَىٰ يَوْمِ
الْقِيَامَةِ لَأَحْتَنِكَنَّ ذُرِّيَّتَهُ إِلَّا قَلِيلًا ﴿62﴾ قَالَ اذْهَبْ فَمَن
تَبِعَكَ مِنْهُمْ فَإِنَّ جَهَنَّمَ جَزَاؤُكُمْ جَزَاءً مَّوْفُورًا ﴿63﴾ وَاسْتَفْزِزْ
مَنِ اسْتَطَعْتَ مِنْهُم بِصَوْتِكَ وَأَجْلِبْ عَلَيْهِم بِخَيْلِكَ
وَرَجِلِكَ وَشَارِكْهُمْ فِي الْأَمْوَالِ وَالْأَوْلَادِ وَعِدْهُمْ
وَمَا يَعِدُهُمُ الشَّيْطَانُ إِلَّا غُرُورًا ﴿64﴾ إِنَّ عِبَادِي لَيْسَ لَكَ عَلَيْهِمْ
سُلْطَانٌ وَكَفَىٰ بِرَبِّكَ وَكِيلًا ﴿65﴾ رَّبُّكُمُ الَّذِي يُزْجِي لَكُمُ
الْفُلْكَ فِي الْبَحْرِ لِتَبْتَغُوا مِن فَضْلِهِ إِنَّهُ كَانَ بِكُمْ رَحِيمًا ﴿66﴾

ثمن

59. Babu abinda ya hana mu aiko da ayoyi (wacce mutanen Makka suka nema) sai don mutan farko sun ƙaryatada ita, mun baiwa Samudawa taguwa aya mabayyaniya suka kafirtada ita suka halaka, Barna aiko da ayoyi (wato mu'ujizozi) sai don ban tsoro.
60. Ka ambata zamanin da mukace dakai haƙiƙa Ubangijinka ya kewaye da mutane (sani da iko, su suna cikin damƙarsa iyar musu da aiken, kadakaji tsoron kowa shine mai kiyayeka daga sharrinsu,) bamu sanyagani wacce muka nuna maka ita ƙarara ba (a daren tafiyar dare,) sai don fitina ga mutanen (Makka) da itaciya abar la'anta (cikin Alƙur'ani Itace Zakkum wacce take fitowa a cikin asalin Jahannama, mun sanya ta fitina garesu Don sun , ce ita wuta kone bishiya take, kaka zata tsuro da itaciya,) muna basu tsoro da ita ban tsoron nan baya kara musu kome illa shisshigi maigirma.

(ASALIN CUTA)

61. Ka ambata zamanin da muka fada ga Mala'iku, "Kuyi sajada ga Annabi Adamu (Alaihisslam, sajadata gaisuwa dasunkuyo,)" sukayi sajada sai Iblis yace, "Ni, shin nayi sajada ga wandaka halitta daga taɓo".
62. Yace. "Bani labari wannan daka fifita shi a kaina (da umarni da sajada a gareshi gashi kuwa na fi shi, ka halicce ni daga wuta,) Wallahi in ka jinkirta min izuwa ranar Alƙiyama zan tunbuke zuriya tasa da halakarwa, sai kaɗan daga garesu (daga wandaka kiyaye su)".
63. Ubangiji yace (dashi,) "Jeka kayi sauraro izuwa lokacin (busar farko,) to, wanda yabika daga cikinsu haƙiƙa jahannama ce sakamakonsu (kai dasu) sakamako abin cikawa.
64. "Tafi da hankalin wandaka samu iko a kansu da muryarka, (ta wakewake da garayu, da dukkan mai kira izuwa saɓon Allah) kai sowa kansu, da dawakanka da satinka, wato mahaya da masu tafiya a (ƙas cikin saɓo,) kai tarayya dasu cikin dukiyoyi abar haramtawa, (kamar ribada kwace,) hakana da 'ya'yaye (ta wajen zina,) kai musu alwashin (cewa ba tashin alƙiyama ba sakamako,) Sheɗan ba yayi musu alƙawarin komai sai ruɗi.

(CIKAKKUN MASANA ANNABAWA DA WALIYYAI)

65. Haƙiƙa bayina (muminai) baka da hannu a kansu, Ubangijinka ya isa wakili a kansu, (mai kiyaye su daga sharrinka kamar Sayyadi, Abubakar Siddiq da Hasanar Basari, da Ibrahim ɗan Adahama, da Abdulkadir Jilani da sauran irinsu har ya zuwa tashin alƙiyama.)

(WANI ABU DAGA NI'IMOMIN ALLAH GAREMU)

66. Ubangijinku shine wanda yake gudanar da jirgi a cikin kogi, don ku nema daga falalarsa (da ciniki ko neman ilimi) haƙiƙa Ubangiji ya kasance mai jinƙai daku, (a cikin hore muku ita.)

وَإِذَا مَسَّكُمُ الضُّرُّ فِي الْبَحْرِ ضَلَّ مَن تَدْعُونَ إِلَّا إِيَّاهُ
فَلَمَّا نَجَّاكُمْ إِلَى الْبَرِّ أَعْرَضْتُمْ وَكَانَ الْإِنسَانُ كَفُورًا ﴿67﴾
أَفَأَمِنتُمْ أَن يَخْسِفَ بِكُمْ جَانِبَ الْبَرِّ أَوْ يُرْسِلَ عَلَيْكُمْ حَاصِبًا
ثُمَّ لَا تَجِدُوا لَكُمْ وَكِيلًا ﴿68﴾ أَمْ أَمِنتُمْ أَن يُعِيدَكُمْ فِيهِ تَارَةً أُخْرَىٰ
فَيُرْسِلَ عَلَيْكُمْ قَاصِفًا مِّنَ الرِّيحِ فَيُغْرِقَكُم بِمَا كَفَرْتُمْ
ثُمَّ لَا تَجِدُوا لَكُمْ عَلَيْنَا بِهِ تَبِيعًا ﴿69﴾ * وَلَقَدْ كَرَّمْنَا بَنِي آدَمَ
وَحَمَلْنَاهُمْ فِي الْبَرِّ وَالْبَحْرِ وَرَزَقْنَاهُم مِّنَ الطَّيِّبَاتِ
وَفَضَّلْنَاهُمْ عَلَىٰ كَثِيرٍ مِّمَّنْ خَلَقْنَا تَفْضِيلًا ﴿70﴾ يَوْمَ نَدْعُوا
كُلَّ أُنَاسٍ بِإِمَامِهِمْ فَمَنْ أُوتِيَ كِتَابَهُ بِيَمِينِهِ فَأُولَٰئِكَ
يَقْرَءُونَ كِتَابَهُمْ وَلَا يُظْلَمُونَ فَتِيلًا ﴿71﴾ وَمَن كَانَ فِي هَٰذِهِ
أَعْمَىٰ فَهُوَ فِي الْآخِرَةِ أَعْمَىٰ وَأَضَلُّ سَبِيلًا ﴿72﴾ وَإِن كَادُوا
لَيَفْتِنُونَكَ عَنِ الَّذِي أَوْحَيْنَا إِلَيْكَ لِتَفْتَرِيَ عَلَيْنَا غَيْرَهُ
وَإِذًا لَّاتَّخَذُوكَ خَلِيلًا ﴿73﴾ وَلَوْلَا أَن ثَبَّتْنَاكَ لَقَدْ كِدتَّ
تَرْكَنُ إِلَيْهِمْ شَيْئًا قَلِيلًا ﴿74﴾ إِذًا لَّأَذَقْنَاكَ ضِعْفَ الْحَيَاةِ
وَضِعْفَ الْمَمَاتِ ثُمَّ لَا تَجِدُ لَكَ عَلَيْنَا نَصِيرًا ﴿75﴾

رُبع

67. Idan tsanani ya same ku a cikin kogi (ko sararin sama tsoron nutsewa ko faɗowa) wanda kuke kira saiya bace muku (nadaga gumaka.) sai Allah (saboda ba mai yaye wannan tsananin sai shi). To yayin daya tserar daku ,(daga nutsewa ko faɗowa ya sada ku) izuwa sarari sai kubijire (ga buran kaɗaita shi). Haƙiƙa mutum ya kasance mai butilcewa (ni'imar Allah).
68. Shin, to kun amince ya kisfe nahiyar sarari daku ,ne? (Kamar Karuna.) ko ya aiko iska mai jifa da tsakwankwani a gareku (kamar mutanen Annabi Luɗu Alaihissalamu,) sannan bazaku sami wakili (ko) mai kiyayeku daga halaka ba.
69. Bari! Shin kun amince mu mayar daku ,cikin kogin nan wani yayi, mu aiko. ƙaƙƙarfar iska a kanku ta nutsar daku ,saboda kafircinku, sannan bazaku sami mai bi biyagareku a kanmu ba (saboda halakar wannan da mukayi muku.)
70. Haƙiƙa mun fifita bilAdama (da ilimi da furuci da daidaiton kira, da tsarkaka bayan mutuwa, da wanin wannan,) mun ɗauke su (a kan dabbobi) a cikin sarari da kogi (a kan jirage da sararin sama a cikin jirgin sama) mun azurta su daga daɗaɗa, mun fifita su a kan yawaici daga abinda muka halitta, (kamar dabbobi da bakwane,) fifitawa.

(SASHIN MATSAYEN RANAR ALƘIYAMA)

71. Ka ambaci ranar da muke kiran kowace al'umma da Annabinta, (a ce ya Ummatu Ibrahim, Ya Ummatu Isa, Ya Ummatu Mu-hammadu alaihimussalamu, shiryagabanin ɓata kuma haka ya mabiyafir'auna ko Numuruzu, ko wane ko wane, shine ranar alƙiyama,) to, duka wanda aka bashi takardarsa a damansa (sune sa'idai, ma'abuta basira a duniya.) Waɗancananka zasu karanta littafinsu baza a zalunce su gwargwadon bawan ɗan ɓalle ba.
72. Wanda ya kasance a cikin wannan duniya makaho (ga buran gaskiya.) to shi a ranar Lahira makaho ne (ga buran hanyar tsira da karatun littafi mafi bacewa turba.(Zamanin da Saƙifawa suka roƙi Annabi mai tsira da amincin Allah ya haramta musu zazansu wato ya mayar dashi hurumi suka nannace masa da nema sai aka saukar da:)
73. Haƙiƙa sun kusa su fitinceka ga buran abinda aka aiko izuwa gareka, domin ka ƙirƙiri waninsa a kanmu, daka aikata wannan dasun riƙe ka badaɗi.
74. Ba don mun tabbatar dakai (a kan gaskiya ba) da haƙiƙa ka kusa ka karkato izuwa garesu karkato kaɗan (saboda tsananin wayansu da nannace-warsu. Wannan aya ta nuna ƙarara cewa Annabi mai tsira da amin-cin Allah bai karkata ba, bai kusa ya karkata ba.
75. Daka karkatada mun ɗanɗana maka ninkin azabar rayuwa, da ninkin azabar rasuwa,sannan bazaka sami wani mai taimako a kanmu ba.

وَإِن كَادُواْ لَيَسْتَفِزُّونَكَ مِنَ اَ۬لْأَرْضِ لِيُخْرِجُوكَ مِنْهَا
وَإِذاً لَّا يَلْبَثُونَ خَلْفَكَ إِلَّا قَلِيلاً ﴿76﴾ سُنَّةَ مَن قَدْ أَرْسَلْنَا قَبْلَكَ
مِن رُّسُلِنَا وَلَا تَجِدُ لِسُنَّتِنَا تَحْوِيلاً ﴿77﴾ أَقِمِ اِ۬لصَّلَوٰةَ لِدُلُوكِ اِ۬لشَّمْسِ
إِلَىٰ غَسَقِ اِ۬ليْلِ وَقُرْءَانَ اَ۬لْفَجْرِ إِنَّ قُرْءَانَ اَ۬لْفَجْرِ كَانَ
مَشْهُوداً ﴿78﴾ وَمِنَ اَ۬ليْلِ فَتَهَجَّدْ بِهِۦ نَافِلَةً لَّكَ عَسَىٰ أَن يَبْعَثَكَ رَبُّكَ
مَقَاماً مَّحْمُوداً ﴿79﴾ وَقُل رَّبِّ أَدْخِلْنِے مُدْخَلَ صِدْقٍ وَأَخْرِجْنِے
مُخْرَجَ صِدْقٍ وَاجْعَل لِّيَ مِن لَّدُنكَ سُلْطَٰناً نَّصِيراً ﴿80﴾
وَقُلْ جَآءَ اَ۬لْحَقُّ وَزَهَقَ اَ۬لْبَٰطِلُ إِنَّ اَ۬لْبَٰطِلَ كَانَ زَهُوقاً ﴿81﴾
وَنُنَزِّلُ مِنَ اَ۬لْقُرْءَانِ مَا هُوَ شِفَآءٌ وَرَحْمَةٌ لِّلْمُؤْمِنِينَ
وَلَا يَزِيدُ اُ۬لظَّٰلِمِينَ إِلَّا خَسَاراً ﴿82﴾ وَإِذَا أَنْعَمْنَا عَلَى اَ۬لْإِنسَٰنِ
أَعْرَضَ وَنَٰٓـَٔا بِجَانِبِهِۦ وَإِذَا مَسَّهُ اُ۬لشَّرُّ كَانَ يَـُٔوساً ﴿83﴾ قُلْ كُلٌّ
يَعْمَلُ عَلَىٰ شَاكِلَتِهِۦ فَرَبُّكُمُۥ أَعْلَمُ بِمَنْ هُوَ أَهْدَىٰ سَبِيلاً ﴿84﴾
* وَيَسْـَٔلُونَكَ عَنِ اِ۬لرُّوحِ قُلِ اِ۬لرُّوحُ مِنْ أَمْرِ رَبِّے
وَمَا أُوتِيتُم مِّنَ اَ۬لْعِلْمِ إِلَّا قَلِيلاً ﴿85﴾ وَلَئِن شِئْنَا لَنَذْهَبَنَّ
بِالذِے أَوْحَيْنَا إِلَيْكَ ثُمَّ لَا تَجِدُ لَكَ بِهِۦ عَلَيْنَا وَكِيلاً ﴿86﴾

ثمن

76. Haƙiƙa sun kusa su girgizar dakai daga ƙasar (Madina wato su fitar da kai) to, yayin nan kuwa (dasun fitar da kai) da bazasu zauna a bayan ta ba sai kaɗan, sannan suhalaka.
77. Al'adar wanda muka aiko gabanka kansu daga manzanninmu bazaka sami musanyawa ba ga al'adarmu.

(NASIHOHI DA GARGADI)

78. Ka tsaida salla (daidai wadaida da sharuɗanta na badini da zahiri tun daga zawalin rana) izuwa duhun dare, (azahar ke nan da la'asar da magaribada lisha,) da sallar alfijir, haƙiƙa sallar alfijir ya kasance abin halarta, (Mala'ikun dare dana rana suna halartarsa.)
79. Daga dare kuma sai kayi sallar Ƙiyamullaili da Alƙur'ani nafila gareka, (wato farilla abar ka-rawa a kanka, saboda wajabcin tahajjudu a kansa.) (matsayin yabo ranar alƙiyama) Ana ƙaunar Ubangijinka ya tasheka a matsayi abin godewa, (mutanen farko dana ƙarshe zasu gode maka, shine matsayin ceto a cikin rabe hukuncin. (Yayin da aka umarce su da hijira sai Allah yace:)
80. Cene "Ubangiji shigar dani (Madina) mashiga na gaskiya ka fitar dani daga Makka) fitarwa ta gaskiya (bazan waiwaye da zuciya izuwa gareta ba,) ka sanya mini hujja mai taimakona (a kan magauta) daga gareka".
81. Ka faɗa (yayin shigarka Makka) "Gaskiya (Itace Musulunci) ta zo, ƙarya (wato kafirci) ta lalace, haƙiƙa ƙarya ta kasance mai sheƙewa" (alhali ya shigeta Sallallahu alaihi wasallama daura da Ka'aba akwai gunki ɗari ukuda sittin (360) ya hadu yana faɗar wancananka har dai duk ta faɗi da goshi da ƙeya. Buhari ya ruwaito shi da Muslim).
82. Muna saukarwa daga (shi) Alƙir'ani wanda yake shine waraka (daga ɓata,) da rahama ga muminai, baya karawa kafirai komai saitaɓewa.
83. Idan mukayi ni'ima bisa mutum (wato kafiri) sai yakan bijire (ga buran godiya) yakan yi nesa da nahiya tasa don girman kai,) idan sharri ya sameshi (wato ƙari da tsanani) saiya kasance mai ɗebe haso daga rahamar Ubangiji.
84. Cene "Kowanne (da mu da ku) yai aiki bisa hanya tasa Ubangijinku shine masani da wanda yafi kowa shiriya (zaiyi masa sakamako).

(HAƘIƘAR RAI)

85. Suna tambayarku, wato Yahudu) haƙiƙar rai (wanda jiki yake rayuwa dashi,) Cene (dasu) "Rai yana daga al'amann Ubangijina, (baku sanshi ba,) ba a baku naɗaga ilimi ba sai kaɗan, dangane da ilimin Allah".)

(ALƘUR'ANI SHINE MU,UJIZA MADAWWAMIYA)

86. Wallahi in mun ga dama zamu tafi da abin nan da muka aiko izuwa gareka (alƙur'ani, mu shafe shi daga ƙiraza da littattafai,) sannan bazaka sami wani wakili a kan tafiyar wannan ba.

إِلَّا رَحْمَةً مِّن رَّبِّكَ إِنَّ فَضْلَهُۥ كَانَ عَلَيْكَ كَبِيراً ﴿87﴾ قُل لَّئِنِ
اِجْتَمَعَتِ الْإِنسُ وَالْجِنُّ عَلَىٰٓ أَن يَأْتُواْ بِمِثْلِ هَٰذَا الْقُرْءَانِ لَا يَأْتُونَ
بِمِثْلِهِۦ وَلَوْ كَانَ بَعْضُهُمْ لِبَعْضٍ ظَهِيراً ﴿88﴾ وَلَقَدْ صَرَّفْنَا
لِلنَّاسِ فِي هَٰذَا الْقُرْءَانِ مِن كُلِّ مَثَلٍ فَأَبَىٰٓ أَكْثَرُ النَّاسِ
إِلَّا كُفُوراً ﴿89﴾ وَقَالُواْ لَن نُّؤْمِنَ لَكَ حَتَّىٰ تُفَجِّرَ لَنَا
مِنَ الْأَرْضِ يَنۢبُوعاً ﴿90﴾ أَوْ تَكُونَ لَكَ جَنَّةٌ مِّن نَّخِيلٍ
وَعِنَبٍ فَتُفَجِّرَ الْأَنْهَٰرَ خِلَٰلَهَا تَفْجِيراً ﴿91﴾ أَوْ تُسْقِطَ السَّمَآءَ
كَمَا زَعَمْتَ عَلَيْنَا كِسَفاً أَوْ تَأْتِيَ بِاللَّهِ وَالْمَلَٰٓئِكَةِ
قَبِيلاً ﴿92﴾ أَوْ يَكُونَ لَكَ بَيْتٌ مِّن زُخْرُفٍ أَوْ تَرْقَىٰ فِي السَّمَآءِ
وَلَن نُّؤْمِنَ لِرُقِيِّكَ حَتَّىٰ تُنَزِّلَ عَلَيْنَا كِتَٰباً نَّقْرَؤُهُۥ
قُلْ سُبْحَانَ رَبِّي هَلْ كُنتُ إِلَّا بَشَراً رَّسُولاً ﴿93﴾ وَمَا مَنَعَ النَّاسَ
أَن يُؤْمِنُوٓاْ إِذْ جَآءَهُمُ الْهُدَىٰٓ إِلَّا أَن قَالُوٓاْ أَبَعَثَ اللَّهُ بَشَراً
رَّسُولاً ﴿94﴾ قُل لَّوْ كَانَ فِي الْأَرْضِ مَلَٰٓئِكَةٌ يَمْشُونَ مُطْمَئِنِّينَ
لَنَزَّلْنَا عَلَيْهِم مِّنَ السَّمَآءِ مَلَكاً رَّسُولاً ﴿95﴾ قُلْ كَفَىٰ بِاللَّهِ شَهِيداً
بَيْنِي وَبَيْنَكُمْ إِنَّهُۥ كَانَ بِعِبَادِهِۦ خَبِيراً بَصِيراً ﴿96﴾

87. Sai dai (mun wanzar dashine) don jinƙai daga Ubangijinka, haƙiƙa falalar Ubangiji ta kasance mai girma a gareka daya saukar dashi a gareka ya baka matsayin yabo, da wanin wancananka na fifikai).
88. Cene "Wallahi da mutane da aljannu zasu tattara, a kan su zoda kamar wannan Alƙur'ani (cikin fasaha da azanci,) bazasu zoda misalin sa ba, koda sashinsu ya kasance a bisa raddi a kan faɗinsu da mun ga dama da mun faɗi kamar wannan.)
89. Haƙiƙa munyi bayani ga mu-tane a cikin wannan Alƙur'ani daga dukkan misali (donsu wa'azantu,) yawaicin mutane suka ki sai kafircewa (da gaskiya).
90. Sukace, "Bazamu gasgatadakai ba,sai ka bubbugo mana da idaniya ta ruwa daga ƙasa,
91. Ko gonar dabino da inabi ta kasance gareka ka bubbugo da ƙoramu ƙarƙashinta bubbugarwa.
92. "Ko ka faɗo da sama (a kanmu) tamfar daka riya yanƙi yanki ko ka zoda Allah da Mala'iku gabada gaba (mugansu ƙarara).
93. Ko ya zama kana da ɗaki na zinare, ko ka hau a cikin sama (da tsani,) bazamu gasgata saboda hawanka ba, sai ka saukar mana da littafi (daga gareta wanda gasgataka yake cikinsa) mu ka-ranta shi. Cene (dasu) "Tsarki Ya tabbatarwa Ubangijina, ni ban kasance ba sai mutum abin aikowa (tamfar sauran manzanni, su ko basa zuwa da aya saida iznin Allah.)

(SHUBUHARSU A CIKIN AIKE DA RADDI A KANSU)

94. Ba abinda ya hana mutane bada gaskiya zamanin da gaskiya tazo musu, sai cewar su "Yanzu Allah ya aiko ɗan Adam jakada (ba Mala'ika ba.")
95. Cene (dasu) "Da Mala'ikune a bayan ƙasa (maimakon ɗan Adam) suke tafiya a nutse da mun saukar da Mala'ika a garesu daga sama jakada, (ba a aiko da jakada izuwa mutane sai daga jinsinsu.) Saboda zance dashiya sauwa ka garesu.
96. Cene "Allah ya isa sheda tsakanina daku ,(a bisa gaskiyata,) Ubangiji masanin badinin bayinsa ne tamfar zahirinsu".

وَمَنْ يَهْدِ اِ۬للَّهُ فَهُوَ اَ۬لْمُهْتَدِۦۖ وَمَنْ يُضْلِلْ فَلَن تَجِدَ لَهُمْ
أَوْلِيَآءَ مِن دُونِهِۦۖ وَنَحْشُرُهُمْ يَوْمَ اَ۬لْقِيَٰمَةِ عَلَىٰ وُجُوهِهِمْ
عُمْياً وَبُكْماً وَصُمّاًۖ مَّأْوَيٰهُمْ جَهَنَّمُۖ كُلَّمَا خَبَتْ زِدْنَٰهُمْ
سَعِيراً ﴿97﴾ ذَٰلِكَ جَزَآؤُهُم بِأَنَّهُمْ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَقَالُوٓاْ أَ۟ذَا
كُنَّا عِظَٰماً وَرُفَٰتاً اِنَّا لَمَبْعُوثُونَ خَلْقاً جَدِيداًۖ ﴿98﴾
حزب
* أَوَلَمْ يَرَوْاْ أَنَّ اَ۬للَّهَ اَ۬لذِے خَلَقَ اَ۬لسَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضَ قَادِرٌ عَلَىٰ
أَنْ يَّخْلُقَ مِثْلَهُمْ وَجَعَلَ لَهُمْ أَجَلاً لَّا رَيْبَ فِيهِۖ فَأَبَى اَ۬لظَّٰلِمُونَ
إِلَّا كُفُوراًۖ ﴿99﴾ قُل لَّوْ أَنتُمْ تَمْلِكُونَ خَزَآئِنَ رَحْمَةِ رَبِّيَ إِذاً لَّأَمْسَكْتُمْ
خَشْيَةَ اَ۬لْإِنفَاقِۖ وَكَانَ اَ۬لْإِنسَٰنُ قَتُوراًۖ ﴿100﴾ وَلَقَدَ اٰتَيْنَا
مُوسَىٰ تِسْعَ ءَايَٰتِۢ بَيِّنَٰتٍۖ فَسْـَٔلْ بَنِےٓ إِسْرَآءِيلَ إِذْ جَآءَهُمْ
فَقَالَ لَهُۥ فِرْعَوْنُ إِنِّے لَأَظُنُّكَ يَٰمُوسَيٰ مَسْحُوراًۖ ﴿101﴾
قَالَ لَقَدْ عَلِمْتَ مَا أَنزَلَ هَٰٓؤُلَآءِ إِلَّا رَبُّ اُ۬لسَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ بَصَآئِرَ
وَإِنِّے لَأَظُنُّكَ يَٰفِرْعَوْنُ مَثْبُوراًۖ ﴿102﴾ فَأَرَادَ أَن يَّسْتَفِزَّهُم
مِّنَ اَ۬لْأَرْضِ فَأَغْرَقْنَٰهُ وَمَن مَّعَهُۥ جَمِيعاًۖ ﴿103﴾ وَقُلْنَا مِنۢ بَعْدِهِۦ لِبَنِےٓ
إِسْرَآءِيلَ اَ۟سْكُنُواْ اُ۬لْأَرْضَۖ فَإِذَا جَآءَ وَعْدُ اُ۬لْأٓخِرَةِ جِئْنَا بِكُمْ لَفِيفاًۖ ﴿104﴾

97. Wanda Allah ya shirye shi shine mai shiriya, wanda ya ɓatar bazaka sami waɗansu majuɓuntada zasu shiryesu ba Allah ba. muna tara su ranar Alƙiyama (suna tafe a kan fuskokinsu makafi, bebaye, kurame. Makomarsu jahannama, ko dayaushe ta huce sai mu ƙara musu zafi da hurawa.
98. Wancananka shine sakamakonsu, saboda kasancewarsu sun kafirtada ayoyinmu sun ci (suna musu da tashin Alƙiyama,) "Yanzu idan mun zama kasusuwa rududdu-gaggu haƙiƙa mu za a tashe mu halitta sabuwa?"
99. Yanzu basa gani haƙiƙa Ubangiji wanda ya halicci sammai da ƙassai (tareda girmansu) mai iko ne bisa ya halicci misalinsu (wato mutane a kan ƙanƙanta) yasanya musu ajali garesu (na mutuwa da tashi,) wanda babu kokonto a cikinsa, sai azzalumai suka ki sai kafircewa.
100. Cene (dasu) "Da cewa ku, kune kuka mallaki taskokin Ubangijina (na arziki da ruwa,) yayin nan da kun yi rowa, don tsoron ciyarwa, kai, haƙiƙa mutum ya kasance mai yawan kwauro".

(RARRASHIN ANNABI MAI TSIRA DA AMINCIN ALLAH)

101. Haƙiƙa mun baiwa Annabi Musa ayoyi guda tara mabayyana, (hannu, sanda, ɗufanu, fara, kwarkwata, kwado, jini, toshewa, fari, (tawayar itatuwa,) Kayi tambayo (Ya Annabi mai tsira da amincin Allah ka tambayi) Bani-Isra'ila zamanin dayazo musu, sai Fir'auna yace (dashi) " Haƙiƙa Ya Kai Musa ni, ina zatonka abin rinjaye ni (bisa hankalinka.)"
102. Sai yace, " Haƙiƙa ka sani ba wanda ya saukar da waɗannan ayoyi sai Ubangijin sammai da ƙassai, don haskaka basira, haƙiƙa ni, ina zatonka yafir'auna halakakke".
103. Shi Fir'auna yanufi ya girgizar da Annabi Musa da mutanensa daga cikin ƙasar Misra muka nutsar dashi da waɗanda suke tare dashi bakiɗaya.
104. Muka faɗa bayansa ga Bani-Isra'ila "Ku zauna ƙasar Misra idan lokacin ta ƙarshe (Itace alƙiyama) yazo, sai mu zodaku ,a tattare (ku dasu)",
105. Da gaskiya muka saukar dashi (alƙur'ani) kuma da gaskiyaya sauka, bamu aiko ka ba face mai albishir ga wanda ya bada gaskiya (da aljanna,) mai gargaɗi (ga wanda ya kafirtada wuta.)
106. Mun saukar dashi Alƙur'ani abin rarrabawa (a cikin shekara ashirin da uku) donka karanta shi ga mutane a bisa nutsuwa, mun saukar dashi saukarwa kaɗan-kaɗan (gwargwadon masalahar bayi.)
107. Cene (da kafirai) "Ku bada gaskiya dashi ko kadaku ,bada gaskiya dashi, (ban tsoro ne garesu,) haƙiƙa waɗanda aka basu ilimi gabansa sune muminai AhlulKitabi, idan ana karanta shi a garesu suna faɗuwa a kan haɓuɓɓansu suna masu sajada, suna cewa Tsarki ya tabbatar wa Ubangijinmu (daga saba alƙawari) haƙiƙa alƙawarin Ubangijinmu (da saukar sa da aiko Annabi mai tsira da amincin Allah abin aikatawane.
108. Suna faɗuwa izuwa haɓuɓɓansu suna masu kuka, alƙur'ani yana ƙara musu ƙanƙandakai (ga Allah.)

(SUNANNAKIN UBANGIJI DARI DAYA BABU)

Manzon Allah ya kasance yana cewa ya Allahu, Ya Rahmanu, sai sukace yana hana mu mu bautawa ubangiji biyu, yana k ran ubangiji wani dabam tare dashi, sai aka saukar da:"

وَبِالْحَقِّ أَنزَلْنَـٰهُ وَبِالْحَقِّ نَزَلَ وَمَآ أَرْسَلْنَـٰكَ إِلَّا مُبَشِّرًا وَنَذِيرًا ﴿105﴾
وَقُرْءَانًا فَرَقْنَـٰهُ لِتَقْرَأَهُۥ عَلَى ٱلنَّاسِ عَلَىٰ مُكْثٍ وَنَزَّلْنَـٰهُ تَنزِيلًا ﴿106﴾
قُلْ ءَامِنُوا۟ بِهِۦٓ أَوْ لَا تُؤْمِنُوٓا۟ إِنَّ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْعِلْمَ مِن قَبْلِهِۦٓ إِذَا يُتْلَىٰ
عَلَيْهِمْ يَخِرُّونَ لِلْأَذْقَانِ سُجَّدًا وَيَقُولُونَ سُبْحَـٰنَ رَبِّنَآ إِن كَانَ وَعْدُ رَبِّنَا
لَمَفْعُولًا ﴿107﴾ وَيَخِرُّونَ لِلْأَذْقَانِ يَبْكُونَ وَيَزِيدُهُمْ خُشُوعًا ۩ ﴿108﴾ سجدة
قُلِ ٱدْعُوا۟ ٱللَّهَ أَوِ ٱدْعُوا۟ ٱلرَّحْمَـٰنَ أَيًّا مَّا تَدْعُوا۟ فَلَهُ ٱلْأَسْمَآءُ ٱلْحُسْنَىٰ
وَلَا تَجْهَرْ بِصَلَاتِكَ وَلَا تُخَافِتْ بِهَا وَٱبْتَغِ بَيْنَ ذَٰلِكَ سَبِيلًا ﴿109﴾
وَقُلِ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِى لَمْ يَتَّخِذْ وَلَدًا وَلَمْ يَكُن لَّهُۥ شَرِيكٌ
فِى ٱلْمُلْكِ وَلَمْ يَكُن لَّهُۥ وَلِىٌّ مِّنَ ٱلذُّلِّ وَكَبِّرْهُ تَكْبِيرًا ﴿110﴾

18 سُورَةُ الْكَهْفِ مَكِّيَّةٌ
وَهِيَ مِائَةٌ وَخَمْسُ ءَايَاتٍ 105

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَـٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ثمن ۞ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ عَلَىٰ عَبْدِهِ ٱلْكِتَـٰبَ وَلَمْ يَجْعَل لَّهُۥ عِوَجًا ﴿1﴾ قَيِّمًا
لِّيُنذِرَ بَأْسًا شَدِيدًا مِّن لَّدُنْهُ وَيُبَشِّرَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ٱلَّذِينَ يَعْمَلُونَ ٱلصَّـٰلِحَـٰتِ أَنَّ
لَهُمْ أَجْرًا حَسَنًا ﴿2﴾ مَّـٰكِثِينَ فِيهِ أَبَدًا ﴿3﴾ وَيُنذِرَ ٱلَّذِينَ قَالُوا۟ ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ وَلَدًا ﴿4﴾

109. Cene (dasu) "Ku Kira Allahu ko Arrahaman (Ku ce Ya Allahu, Ya rahmanu,) kowanne kuka kirawo to, (Kyakkyawa ne,) sunannaki kyawawa suna ga Allah, (to wađannan suna daga cikinsu, tamfar dayazo cikin Hadisi, shine Allah wanda babu wani abin bautawa da gaskıya sai shi, Mai jinƙai da man-yamanyan ni'imomı, mai jinƙai da ƙanƙananan ni'imomi, Sarki mana llaki, mai tsarkaka ga buran dukkan laifi, lafiyayye sumul, mai amintar da bayinsa, mai ganin bayinsa basa ganinsa, mabuwayi, mai đorin karaya, mai jin girma, mahalicci, mai ƙera halitta, mai kamanta halitta, mai yawan gafara, mai yawan rinjaye, mai yawan baiwa, mai yawan azurta wa, mai yawan buđi, mai yawan sani, mai karɓar rayuka da arziki, mai yalwatawar arziki, mai ƙasƙanta wanda yaga dama, mai đaga wanda yaga dama, mai buway-anta wanda yaga dama, mai wulaƙanta wanda yaga dama, mai jin komai, mai ganin kmai, mai hukunci, Adalin Sarki, mai taushi, masanin bađinin al'amura, mai jinkirin azaba ga wanda ya cancanceta, mai girman zati, mai yawan gafara, mai sakamako da yawa ga aiki ƙanƙane, mađaukaki, mai girma, mai kiyayc halitta, mai basu abinci, wanda ya ishi kowa, mai girman alƙadari, mai karim- ci, (ya bayar ba sai an tambaye shi ba,) mai la'akari da bayi, maji roƙon bayi, mayalwacin kyauta, Gwani, mai soyar da kansa ga bayinsa, mai girman daraja, mai aiko manzanni alaihimussalamu, wanda yake mahalarci ga komai, tabbatacce, wakilin kowa, mai ƙarfin bađini, mai ƙarfin zahiri, waliyyin kowa, abin godiyar kowa, mai kiyayewa ga aikin kowa, mai fara halitta, mai maida ita bayan ta mutu, mai rayawa, mai kashewa, Rayayyen Sarki, mai tokare sammai da ƙassai, wanda ba abinda bashi dashi, mai ci-kakkiyar daraja, mađayanci, abin nufi da bukata, mai iko, mai gwaninta, mai gabatar da wanda yaga dama, mai jinkirta wanda yaga dama, na farko, na ƙarshe, mabayyani da aiki, ɓoyayye ga zahiri, majiɓunci, mai đaukaka, mai aikin alheri, mai karɓar tuba, mai azaba, mai afuwa, mai tsananin jinƙai, ma-mallakin mulki, ma'abocin girma da alheri, mai adalci, mai tara dukkan cika, wadatacce, mai wadatarwa, mai hana wanda yaga dama, mai cutar wanda yaga dama, mai amfanin wanda yaga dama, haske, mai shıryarwa, mai ƙagar mutane (bada misali daya duba ba), mai wanzuwa bayan kowa, magajin kowa, mai shiryar da bayi, mai yawan haƙuri,; Turmuzi ya ruwaito wannan Hadisi. Yayi kyau a sa Jalla-Jalaluhu a ƙarshen kowane suna). Kadaka bayyana da karatunka, (mushrikai suji su zage ka, su zagi Alƙur'ani da wanda ya saukar dashi.) Kadaka ɓoye da karatun Ka (don Sahabbanka su am-fana,) Ka nufi hanya matsakan ciya tsakanin bayyanawa da boyewa".

110. Ka ce, "Godiya ta tabbata ga Allah wanda bai riƙi đa ba, bashi da abokin tarayya a cikin mulki (Allantaka,) bashi da wani mujibinci dazai taimakc shi daga wulaƙanci, ka girmama shi girmama wa.

Suratul Kahafi

A Makka Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Dari Da Biyar (105)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba đaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

(Wato wannan sura Itace tayi magana a kan Sufanci dasufaye ta kowacce fuska, muminan haƙiƙa su kula da ita. Tayi magana kan Alƙur'ani da tasirinsa da ƙissar ma'abuta kogo da abinda yake cikinta na iznace-iznace, da fuskan-tarwa mai amfani, da sanya misali na aiki ga wanda ya rudu da duniya tareda gargađarwa da ranar Alƙiyama da ƙissar Annabi Musa tareda Halliru Alaihimasalamu da jaw-abi a kan rai, da Zilƙarnaini.)

1. Godiya ta tabbata ga Allah wanda ya saukar da Alƙur'ani a bisa bawansa (Annabi Muhammadu mai tsira da amincin Allah,) bai sanya karkata a ciki ba, (wato saɓani. Ko warwarewar magana.)
2. Madaidaici, domin ya tsoratar da Kafirai da wannan Alƙur'ani azaba mai rađađi daga Ubangiji, yayi wa muminai albishir wađanda suke aikata ayyuka na-gargaru, haƙiƙa lada mai kyau yana garesu.
3. Masu dauwama a cikinsa har abada (shine aljanna.)
4. Ya tsoratar da wađanda Sukace, "Ubangiji ya riƙi đa".

مَّا لَهُم بِهِۦ مِنْ عِلْمٍ وَلَا لِءَابَآئِهِمْ كَبُرَتْ كَلِمَةً تَخْرُجُ مِنْ
أَفْوَٰهِهِمْ إِن يَقُولُونَ إِلَّا كَذِبًا ۝5 فَلَعَلَّكَ بَٰخِعٌ
نَّفْسَكَ عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِمْ إِن لَّمْ يُؤْمِنُواْ بِهَٰذَا ٱلْحَدِيثِ أَسَفًا ۝6
إِنَّا جَعَلْنَا مَا عَلَى ٱلْأَرْضِ زِينَةً لَّهَا لِنَبْلُوَهُمْ أَيُّهُمْ أَحْسَنُ عَمَلًا ۝7
وَإِنَّا لَجَٰعِلُونَ مَا عَلَيْهَا صَعِيدًا جُرُزًا ۝8 أَمْ حَسِبْتَ أَنَّ
أَصْحَٰبَ ٱلْكَهْفِ وَٱلرَّقِيمِ كَانُواْ مِنْ ءَايَٰتِنَا عَجَبًا ۝9
إِذْ أَوَى ٱلْفِتْيَةُ إِلَى ٱلْكَهْفِ فَقَالُواْ رَبَّنَآ ءَاتِنَا مِن لَّدُنكَ
رَحْمَةً وَهَيِّئْ لَنَا مِنْ أَمْرِنَا رَشَدًا ۝10 فَضَرَبْنَا عَلَىٰٓ ءَاذَانِهِمْ
فِى ٱلْكَهْفِ سِنِينَ عَدَدًا ۝11 ثُمَّ بَعَثْنَٰهُمْ لِنَعْلَمَ أَىُّ
ٱلْحِزْبَيْنِ أَحْصَىٰ لِمَا لَبِثُوٓاْ أَمَدًا ۝12 نَّحْنُ نَقُصُّ عَلَيْكَ
نَبَأَهُم بِٱلْحَقِّ إِنَّهُمْ فِتْيَةٌ ءَامَنُواْ بِرَبِّهِمْ وَزِدْنَٰهُمْ هُدًى ۝13
وَرَبَطْنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ إِذْ قَامُواْ فَقَالُواْ رَبُّنَا رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ
لَن نَّدْعُوَاْ مِن دُونِهِۦٓ إِلَٰهًا لَّقَدْ قُلْنَآ إِذًا شَطَطًا ۝14
هَٰٓؤُلَآءِ قَوْمُنَا ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ ءَالِهَةً لَّوْلَا يَأْتُونَ عَلَيْهِم
بِسُلْطَٰنٍۭ بَيِّنٍ فَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا ۝15

5. Basu da sani ko ƙanƙane da wannan magana, hakana iyay-ensu, kalma da take fita daga bakunansu ta girmama , basa faɗa (a cikin wancananka) sai ƙarya.
6. Watakila kai zaka halakar da kanka ne a bisa gurabansu, (wato bayan juyawarsu ga buranka,) in basu gasgatada wannan Alƙur'ani ba, don baƙin ciki, (saboda kwaɗayinka bisa imaninsu.)
7. Haƙiƙa mu mun sanya abinda yake ban ƙasa (na mai rai da tsiri da Itace da ƙoramu da wanin wannan) ado ga ƙasa, don mu jarrabi mutane mu ga wannenensune mafi kyaun aiki.
8. Haƙiƙa mu zamu sanya abinda yake kanta dandaƙaƙƙe ƙeƙashasshe.

(KISSAR MA'ABUTA KOGO)

9. To, bari! Shin ka zaci ma'abuta kogon dutse da Allon (da aka rubuta sunannakinsu a ciki da nasaba tasu. Haƙiƙa an tambayi Annabi mai tsira da amincin Allah ƙissarsu,) Sun kasance ma-maki ne daga cikin ayoyinmu, (ba tareda sauran ayoyi ba? A'a! basu kasance su kaɗai abin mana ki ba.)
10. Ka ambata zamanin da cikakkun samari suka tattara izuwa kogo, (wato masu cikakken imani,) sukace Ubangijinmu bamu jinƙai daga gareka ka shirya mana shirya daga lamarinmu.
11. To, sai muka sanya barci a kan kunnuwansu a cikin kogo shekaru ababan ƙirgawa.
12. Sannan muka tashe su domin mu nuna a gani waɗanne ne daga cikin jama'ar nan guda biyu (masu saɓani a cikin muddar zamansu) ya kiyaye matuka ga zamansu.
13. Mune muke karanta labarinsu a gareka da gaskiya, haƙiƙa Sudai samari ne da suka bada gaskiya da ubangijinsu muka kara musu shiriya.
14. Muka ɗaure a kan zukatansu (wato muka ƙarfafeta a kan faɗar gaskiya,) yayin da suka tsaya (nan gaba ga sarkinsu, alhali ya umarce su da sajada ga gumaka,) Sukace, "Ubangijinmu shine ubangijin sammai da ƙassai, bazamu bautawa wani ubangiji, bashi ba har abada, haƙiƙa mun faɗi magana mai fai fa yewa a cikin kafirci yayin nan in mun bautawa wanin ubangiji ba Allah ba (takaɗiran.)
15. "Waɗannan mutanen sun riƙi wani abin bautawa ba Allah ba, donme basu zoda hujja mabayyaniya a kansu ba, ba mafi zalunci daga wanda ya ƙagi ƙarya bisa Ubangiji" (ya dangana abokin tarayyagareshi) (sai ba'alin samarin yace ga ba'ali):

وَإِذِ اِعْتَزَلْتُمُوهُمْ وَمَا يَعْبُدُونَ إِلَّا اَللَّهَ فَأْوُۥٓاْ إِلَى اَلْكَهْفِ
يَنشُرْ لَكُمْ رَبُّكُم مِّن رَّحْمَتِهِۦ وَيُهَيِّئْ لَكُم مِّنْ أَمْرِكُم مَّرْفِقاً ﴿16﴾
* وَتَرَى اَلشَّمْسَ إِذَا طَلَعَت تَّزَّاوَرُ عَن كَهْفِهِمْ ذَاتَ اَلْيَمِينِ
وَإِذَا غَرَبَت تَّقْرِضُهُمْ ذَاتَ اَلشِّمَالِ وَهُمْ فِي فَجْوَةٍ مِّنْهُ
ذَٰلِكَ مِنْ ءَايَٰتِ اِ۬للَّهِ مَنْ يَّهْدِ اِ۬للَّهُ فَهُوَ اَلْمُهْتَدِۦ وَمَنْ يُّضْلِلْ
فَلَن تَجِدَ لَهُۥ وَلِيّاً مُّرْشِداً ﴿17﴾ وَتَحْسِبُهُمْ أَيْقَاظاً وَهُمْ رُقُودٌ
وَنُقَلِّبُهُمْ ذَاتَ اَلْيَمِينِ وَذَاتَ اَلشِّمَالِ وَكَلْبُهُم بَٰسِطٌ
ذِرَاعَيْهِ بِالْوَصِيدِ لَوِ اِطَّلَعْتَ عَلَيْهِمْ لَوَلَّيْتَ مِنْهُمْ فِرَاراً
وَلَمُلِّئْتَ مِنْهُمْ رُعْباً ﴿18﴾ وَكَذَٰلِكَ بَعَثْنَٰهُمْ لِيَتَسَآءَلُواْ بَيْنَهُمْ
قَالَ قَآئِلٌ مِّنْهُمْ كَمْ لَبِثْتُمْ قَالُواْ لَبِثْنَا يَوْماً أَوْ بَعْضَ يَوْمٍ
قَالُواْ رَبُّكُمْ أَعْلَمُ بِمَا لَبِثْتُمْ فَابْعَثُواْ أَحَدَكُم بِوَرِقِكُمْ
هَٰذِهِۦ إِلَى اَلْمَدِينَةِ فَلْيَنظُرْ أَيُّهَا أَزْكَىٰ طَعَاماً
فَلْيَأْتِكُم بِرِزْقٍ مِّنْهُ وَلْيَتَلَطَّفْ وَلَا يُشْعِرَنَّ بِكُمْ
أَحَداً ﴿19﴾ إِنَّهُمْ إِن يَظْهَرُواْ عَلَيْكُمْ يَرْجُمُوكُمْ
أَوْ يُعِيدُوكُمْ فِي مِلَّتِهِمْ وَلَن تُفْلِحُوٓاْ إِذاً أَبَداً ﴿20﴾

ربع

16. "Tun da kuka janye musu da abinda suke bautawa ba Allah, ba, to, ku tattara izuwa kogo, Ubangijinku ya kwarara muku daga rahamarsa ya shirya muku jinƙai daga al'amarinku, (na kalacen safe dayamma.")
17. Kana ganin rana idan ta hudo, tana karkacewa ga buran kogonsu nahiyar dama, idan ta faɗi tana barinsu nahiyar hagun, (wato bata tabasu ko kaɗan,) su suna cikin wani faski daga kogon, (iska mai laushi tana samunsu.) Wannan abin ambato yana daga ayoyin Allah, wanda Allah ya shirye shi, shine shiryayye, wanda Allah ya ɓatar dashi bazaka sami waliyyi mai shiryarwa gareshi ba.

(FALALAR MURIDAN SHAIHUNNAI)

18. Kana zaton su daka gansu idan-dunan su biyu saboda idandu-nansu a buɗe suke, alhali su masu barci ne muna juya su dama da hauni don kada ƙasa ta ci namansu, karensu ya miƙe hannayensa a farfajiyar kogo, (sun kasance idan sun juya sai yajuya taredasu, wato shi yana kamar su a cikin barci da farke. Wannan aya ta nuna falalar dan-gantuwa izuwa ahlullahi, don shi wannan kare ga abinda ya samu a duniya, a lahira kuma zai shiga aljanna, duba Sawii a wannan guri) Da kayi tsinkaye a garesu daka girka aguje don gudu daga garesu da an cikaka da far gabadaga garesu.
19. Tamfar da muka aikata abin nan da muka ambata dasu hakana muka tashe su donsu tambayi junansu (da halinsu da tsawon zamansu,) mai faɗa daga cikinsu yace,"Nawa kuka zauna", Sukace, "Mun zauna wuni ko rabin wuni", (saboda sun shiga kogon yayin hudowar rana an tashe su yayin faɗuwarta, sai suka zaci faɗuwar wannan rana faɗuwar ranar shigarsu ce, sannan) sukace (Suna masu saura-ro a cikin wannan) "Ubangijinkune masani da gwargwadon zaman ku, to, ku aiki ɗayan kuda azurfarku wannan izuwa cikin gari, (wato sunan garin Darasusa a yau, ya duba wannenanta yafi kyaun abinci yazo mukuda arziki daga gareshi, ya tausasa kwarai ta wajen hila kada ya sanar da kowa da ku.
20. " Haƙiƙa su in sun yi tsinkaye a kanku zasu jefe kuda ɗuwarwatsu, ko su maisheku cikin addininsu bazaku rabauta ba yayin nan har abada.

وَكَذَٰلِكَ أَعْثَرْنَا عَلَيْهِمْ لِيَعْلَمُوٓاْ أَنَّ وَعْدَ اَللَّهِ حَقٞ وَأَنَّ اَلسَّاعَةَ
لَا رَيْبَ فِيهَآ إِذْ يَتَنَٰزَعُونَ بَيْنَهُمُۥٓ أَمْرَهُمْ فَقَالُواْ اُبْنُواْ
عَلَيْهِم بُنْيَٰناٗ رَّبُّهُمُۥٓ أَعْلَمُ بِهِمْ قَالَ اَلذِينَ غَلَبُواْ عَلَىٰٓ أَمْرِهِمْ
لَنَتَّخِذَنَّ عَلَيْهِم مَّسْجِداٗ ﴿21﴾ سَيَقُولُونَ ثَلَٰثَةٞ رَّابِعُهُمْ
كَلْبُهُمْ وَيَقُولُونَ خَمْسَةٞ سَادِسُهُمْ كَلْبُهُمْ رَجْماَۢ بِالْغَيْبِ
وَيَقُولُونَ سَبْعَةٞ وَثَامِنُهُمْ كَلْبُهُمْ قُل رَّبِّيَ أَعْلَمُ بِعِدَّتِهِم
مَّا يَعْلَمُهُمُۥٓ إِلَّا قَلِيلٞ * فَلَا تُمَارِ فِيهِمُۥٓ إِلَّا مِرَآءٗ ظَٰهِراٗ ثمن
وَلَا تَسْتَفْتِ فِيهِم مِّنْهُمُۥٓ أَحَداٗ ﴿22﴾ وَلَا تَقُولَنَّ لِشَاْےْءٍ اِنِّے فَاعِلٞ
ذَٰلِكَ غَداً ﴿23﴾ إِلَّآ أَنْ يَشَآءَ اَللَّهُ وَاذْكُر رَّبَّكَ إِذَا نَسِيتَ
وَقُلْ عَسَىٰٓ أَنْ يَهْدِيَنِۦ رَبِّے لِأَقْرَبَ مِنْ هَٰذَا رَشَداٗ ﴿24﴾
وَلَبِثُواْ فِے كَهْفِهِمْ ثَلَٰثَ مِاْئَةٖ سِنِينَ وَازْدَادُواْ تِسْعاٗ ﴿25﴾
قُلِ اِللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا لَبِثُواْ لَهُۥ غَيْبُ اُلسَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ
أَبْصِرْ بِهِۦ وَأَسْمِعْ مَا لَهُم مِّن دُونِهِۦ مِن وَلِيّٖ وَلَا يُشْرِكُ
فِے حُكْمِهِۦٓ أَحَداٗ ﴿26﴾ وَاتْلُ مَآ أُوحِيَ إِلَيْكَ مِن كِتَابِ رَبِّكَ
لَا مُبَدِّلَ لِكَلِمَٰتِهِۦ وَلَن تَجِدَ مِن دُونِهِۦ مُلْتَحَداٗ ﴿27﴾

21. Tamfar da muka tashe su hakana muka tsinkayar da mutanensu da muminai a kansu don mutanensu su san haƙiƙa r alƙawarin Allah (da tashin alƙiyama) gaskiya ne, (saboda cewa mai iko a bisa battar (wato samusu barci dasu lokaci mai tsawo da wanzar dasu a kan halinsu ba tareda ci ba, mai iko ne a bisa raya matattu,) haƙiƙa alƙiyama kuma ba kokonto a cikinta, lokacin da (muminai da kafirai) suke jayayyar al'amarin samarin nan a tsakaninsu (a cikin gini daura dasu) sai kafirai suka ce"Ku gina gini daura dasu (dazai suturce su) Ubangijinsune masani dasu, waɗanda sukayi rinjaye a kan al'amarin samarin nan (sune muminai). Sukace "Lallai zamu riƙi masallaci daura dasu, (a dinga salla a cikinsa" aka aikata wannan a bisa kofar kogon.)

22. Da sannu (masu jayayya a cikin adadin samarin nan a zamanin Annabi mai tsira da amincin Allah) ba'alinsu zaice su "ukune na huɗunsu karensu", ba'alinsu zaice "su biyar ne na shidansu karensu", (Waɗannan) maganganu guda biyu na Nasaran Najrana ne) don jifa a cikin duhu, muminai zasu ce "Su bakwai ne na takwas ɗinsu karensu". Cene "Ubangiji ne masani da ƙirgarsu,ba wanda yasan su sai kaɗan". (Ibn Abbas yace ni ina daga cikin kaɗan din yace su bakwai ne. Sunannakin su Maksalmina, Tamliha, Mardunasu, Nayunasu, sarayulasu, Zunawanisu, falyastaɗ'-yunasu, shine makiyayi, karensu ƙiɗimiru), idan an rubuta sunannakin waɗannan Waliyyai akayi kafi a cikin gidasuna hana gobara ko sata ko nutsewar jirgi. Kuma tana maganin kukan yara da haɓoje da ciwon kai, ana ɗaura wa a hannun dama, tana maganin aljana (Inna-uwasu) da abubuwa da dama) duba Sawii.

23. Kada kayi jayayya a kansu sai jayayya mabayyaniya, kadaka nemi fatawar ɗaya daga cikinsu (yahudawa mutanen Makka sun tambaye shi mahallin Asahabul-kahfi yace zan baku labari dashi gobe, bai ce in Allah ya yarda ba, sai Allah yace:)

24. Kada kace da wani abu "Ni zan aikata abu kaza gobe" sai ka haɗa da in Allah ya yarda, ambaci Ubangijinka (wato rataye shi da ganin damar Ubangiji) in ka mance (matukar kana wan-nan mazaunin) Cene "Ina ƙaunar Ubangiji ya shirye ni izuwa mafi kusa daga wannan shiryarwa (Allah ko ya aikata masa haka ɗin.)

25. Sun zauna cikin kogonsu shekara ɗari uku (waɗannan shekaru gurin ma'abota ƙogo suna bin lissafin rana ne, za a ƙara shekaru tara a kan lissafin Larabawa da yake bin wata, saboda haka allah yace) suka ƙara tara (a kan ɗari uku.)

26. Cene "Allah ne masani da gwargwadon abinda suka zauna. Gaibun sammai da ƙassaina ga Allah, Allah da gani yake, Allah da ji yake, mutanen sama dana ƙasa basu da wani waliyyi ba Allah ba baya tara kowa cikin hukuncinsa (saboda shi mawadaci ne ga buran abokin tarayya.)

(FUSKANCE-FUSKANCE GA MANZON ALLAH MAI TSIRA DA AMINCIN ALLAH)

27. Karanta abinda aka aiko izuwa gareka na littafin Ubangijinka, ba mai misanya kalmominsa, bazaka sami mafaka ba bashi ba.

وَاصْبِرْ نَفْسَكَ مَعَ الَّذِينَ يَدْعُونَ رَبَّهُم بِالْغَدَوٰةِ وَالْعَشِيِّ
يُرِيدُونَ وَجْهَهُۥ وَلَا تَعْدُ عَيْنَاكَ عَنْهُمْ تُرِيدُ زِينَةَ الْحَيَوٰةِ
الدُّنْيَا وَلَا تُطِعْ مَنْ أَغْفَلْنَا قَلْبَهُۥ عَن ذِكْرِنَا وَاتَّبَعَ هَوَىٰهُ
وَكَانَ أَمْرُهُۥ فُرُطًا ﴿28﴾ وَقُلِ الْحَقُّ مِن رَّبِّكُمْ فَمَن شَآءَ فَلْيُؤْمِن
وَمَن شَآءَ فَلْيَكْفُرْ إِنَّا أَعْتَدْنَا لِلظَّٰلِمِينَ نَارًا أَحَاطَ بِهِمْ سُرَادِقُهَا
وَإِن يَسْتَغِيثُوا يُغَاثُوا بِمَآءٍ كَالْمُهْلِ يَشْوِي الْوُجُوهَ بِئْسَ الشَّرَابُ
وَسَآءَتْ مُرْتَفَقًا ﴿29﴾ إِنَّ الَّذِينَ ءَامَنُوا وَعَمِلُوا الصَّٰلِحَٰتِ إِنَّا لَا نُضِيعُ
أَجْرَ مَنْ أَحْسَنَ عَمَلًا ﴿30﴾ أُولَٰٓئِكَ لَهُمْ جَنَّٰتُ عَدْنٍ تَجْرِي مِن تَحْتِهِمُ
الْأَنْهَٰرُ يُحَلَّوْنَ فِيهَا مِنْ أَسَاوِرَ مِن ذَهَبٍ وَيَلْبَسُونَ ثِيَابًا
خُضْرًا مِّن سُندُسٍ وَإِسْتَبْرَقٍ مُّتَّكِـِٔينَ فِيهَا عَلَى الْأَرَآئِكِ
نِعْمَ الثَّوَابُ وَحَسُنَتْ مُرْتَفَقًا ﴿31﴾ * وَاضْرِبْ لَهُم مَّثَلًا ربع
رَّجُلَيْنِ جَعَلْنَا لِأَحَدِهِمَا جَنَّتَيْنِ مِنْ أَعْنَٰبٍ وَحَفَفْنَٰهُمَا
بِنَخْلٍ وَجَعَلْنَا بَيْنَهُمَا زَرْعًا كِلْتَا الْجَنَّتَيْنِ ءَاتَتْ أُكُلَهَا
وَلَمْ تَظْلِم مِّنْهُ شَيْـًٔا وَفَجَّرْنَا خِلَٰلَهُمَا نَهَرًا ﴿32﴾ وَكَانَ لَهُۥ ثُمُرٌ
فَقَالَ لِصَٰحِبِهِۦ وَهُوَ يُحَاوِرُهُۥٓ أَنَا أَكْثَرُ مِنكَ مَالًا وَأَعَزُّ نَفَرًا ﴿33﴾

(UMARNI DA ABUTAN DUKKAN MAGASGACI A CIKIN ALLAH,SUFAYE DA IRINSU)

28. Ka tsare kanka tareda wađanda suke bautawa ubangijinsu safiya dayammaci, suna nufin Zatin Allah da ibada tasu, (ba wani abu nadaga bukace-bukacen duniya ba, ko lahira, bal! Sai Zatin Allah kawai suke nufi,wađannan sune haƙiƙar Fuƙara'u, sune kuma Muridai,) kadaka juyar da idandunanka ga buran abokantaka tasu, kana nufin ƙawar duniya, kadaka bi wanda muka rabkanar da zuciyarsa ga buran ambatonmu, (Alƙur'ani da sauran zikirai, shine Uyainatu đan Hisnu Alfazari, da abokansa) a da can, a yanzu kuma (shine dukkan mai da'awar "Saƙafa - asariyya" sađanin Alƙur'ani mai tsarki da abinda Allah ya ladabtar da Sahabban Annabi mai tsira da amincin Allah) Ance wannan aya ta sauka ne cikin As'habul-Suffati su đari bakwai ne a cikin masallacin Manzon Allah mai tsira da amincin Allah, basa fita izuwa ciniki ko noma ko kiwo, zaman salla kawai suke a cikin masallaci, yayin data sauka sai Annabi mai tsira da aminci yace: godiya ta tabbata ga Allah wanda yasanya cikin al'ummata wađanda aka umarce ni in đaure kaina taredasu, wannan aya Itace asalin Sufanci dasufaye a cikin alƙur'ani, Allah ka sanya mu cikin su, ka azurta mana abotar su ka karɓi ranmu a hanyarsu, kayi wa "yan bayanmu haka don girman zatinka da Annabinka mai tsira da aminci, Amin.) Yabi son zuciyarsa a cikin shirka al'amarinsa ya kasance faifayewa.

29. Cene (dashi da sahabbansa, to, wannan Alƙur'ani) shine gaskiya daga ubangijinku wanda yaga dama ya bada gaskiya wanda yaga dama ya kafirta, (firgitarwa ne garesu) haƙiƙa mu, mun tanaji wuta ga kafirai, wacce lokonta ya kewaye dasu in sun nemi taimako a taimaka mu su da ruwa kamar dago-dago na mai da yake ƙone fuskoki (idan an kusanta izuwa gareta,) tur abin sha (wannan dago -dago,) tir! da wuta matashin kai. (ALLAH BAYA TOZARTA AIKIN MAI AIKI NAGARI)

30. Haƙiƙa wađanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru, haƙiƙa Barna tozarta ladan wandayai aiki, (wato Barna tozarta ladansu.)

31. Wađancananka aljannar zama ta tabbata a garesu, ƙoramu tana gudana ƙarƙashinsu anayi musu ado a cikinta na kwandagai, na zinare, suna đaura tufafu kwarra na sundusu (arafiyan dibaja) da istabraku (kakkauran dibaji), suna masu tasa hannu a cikinta a kan gadajen mulki, Madalla sakamako aljanna! Madalla wurin tada hannu!!

(MISALI GA WANDA YA RUDU DA DUNIYA)

32. Sanya wa kafirai misali tareda muminai mutum biyu muka sanya gona guda biyu ga đayansu wato kafirin, gona biyu ta inabai, muka kewayesu da dabinai muka sanya hatsi tsakaninsu da ake abinci dashi.

33. Kowace đaya daga gonakan nan guda biyu ta bada amfaninta, (wato amfanin yayi kyau) bata tauye kome daga gareshi ba, muka bubbugar da ƙorama dasuke gudana a ƙarƙashinsu.

وَدَخَلَ جَنَّتَهُۥ وَهُوَ ظَالِمٞ لِّنَفۡسِهِۦ قَالَ مَآ أَظُنُّ أَن تَبِيدَ هَٰذِهِۦٓ
أَبَدٗا ﴿34﴾ وَمَآ أَظُنُّ ٱلسَّاعَةَ قَآئِمَةٗ وَلَئِن رُّدِدتُّ إِلَىٰ رَبِّيَ لَأَجِدَنَّ
خَيۡرٗا مِّنۡهُمَا مُنقَلَبٗا ﴿35﴾ قَالَ لَهُۥ صَاحِبُهُۥ وَهُوَ يُحَاوِرُهُۥٓ أَكَفَرۡتَ
بِٱلَّذِي خَلَقَكَ مِن تُرَابٖ ثُمَّ مِن نُّطۡفَةٖ ثُمَّ سَوَّىٰكَ رَجُلٗا ﴿36﴾
لَّٰكِنَّا۠ هُوَ ٱللَّهُ رَبِّي وَلَآ أُشۡرِكُ بِرَبِّيَ أَحَدٗا ﴿37﴾ وَلَوۡلَآ إِذۡ
دَخَلۡتَ جَنَّتَكَ قُلۡتَ مَا شَآءَ ٱللَّهُ لَا قُوَّةَ إِلَّا بِٱللَّهِ إِن تَرَنِ
أَنَا أَقَلَّ مِنكَ مَالٗا وَوَلَدٗا ﴿38﴾ فَعَسَىٰ رَبِّيَ أَن يُؤۡتِيَنِ خَيۡرٗا مِّن
جَنَّتِكَ وَيُرۡسِلَ عَلَيۡهَا حُسۡبَانٗا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ فَتُصۡبِحَ صَعِيدٗا زَلَقًا ﴿39﴾
أَوۡ يُصۡبِحَ مَآؤُهَا غَوۡرٗا فَلَن تَسۡتَطِيعَ لَهُۥ طَلَبٗا ﴿40﴾ وَأُحِيطَ بِثَمَرِهِۦ
فَأَصۡبَحَ يُقَلِّبُ كَفَّيۡهِ عَلَىٰ مَآ أَنفَقَ فِيهَا وَهِيَ خَاوِيَةٌ عَلَىٰ عُرُوشِهَا
وَيَقُولُ يَٰلَيۡتَنِي لَمۡ أُشۡرِكۡ بِرَبِّيَ أَحَدٗا ﴿41﴾ وَلَمۡ تَكُن لَّهُۥ فِئَةٞ يَنصُرُونَهُۥ
مِن دُونِ ٱللَّهِ وَمَا كَانَ مُنتَصِرًا ﴿42﴾ هُنَالِكَ ٱلۡوَلَٰيَةُ لِلَّهِ ٱلۡحَقِّ
هُوَ خَيۡرٞ ثَوَابٗا وَخَيۡرٌ عُقۡبٗا ﴿43﴾ ۞ وَٱضۡرِبۡ لَهُم مَّثَلَ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا
كَمَآءٍ أَنزَلۡنَٰهُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَٱخۡتَلَطَ بِهِۦ نَبَاتُ ٱلۡأَرۡضِ
فَأَصۡبَحَ هَشِيمٗا تَذۡرُوهُ ٱلرِّيَٰحُ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ مُّقۡتَدِرًا ﴿44﴾

ثمن

34. Kuma yana da amfanin gona tareda wadannan gonakai guda biyu, saiya fada ga abokinsa (mumini) alhali yana ansheshenivar magana a gareshi (wato ya nai masa tutiya,) ni, na fi ka yawan dukiya, na fi ka girman dangi.
35. Ya shiga gonarsa (da abokin nan nasa, yana kewaya dashi a cikinta, yana nuna masa amfanin-ta,) alhali shi ko mai zalunta ne ga kansa (da kafirci,) yace bana zaton wannan gona tawa zata kare har abada, bana zaton alkiyama zata tashi, Wallahi in an koma dani izuwa Ubangijina a lahira (kamar da kake riyawa,) Lallai zan sami makoma mafificiya daga gareta.
36. Abokinsa (mumini) yace dashi, alhali yana amsa masa magana, yanzu ka kafirtada wanda ya halicce ka daga turbaya, (domin Annabi Adamu mai tsira da amiricin Allah daga turbaya aka halicce shi) sannan kuma daga maniyyi. Sannan ya daidaita ka mutum!
37. Sai dai ni! Shi wannan sha'ani ni ina ce dakai "Allah ne Ubangijina, bana tara kowa tareda ubangijina (cikin bauta.)
38. Donme a yayin daka shiga gonarka bakace (yayin da kake tunkaho da ita wannan) abinda Allah ya nufa karfi bisa samar da alheri na wannan gona saida karfin Allah, a cikin Hadisi wanda aka bashi wani alheri na iyali ko na dukiya yace mashaallahu Lakuwata illa billahi, bazai ga abin ki a cikinsa ba wato zai masa maganin hau) in ka gan ni ni mafi karancin dukiya da "ya"ya daga gareka.
39. Ina kaunar Ubangijina ya bani mafifici daga gonarka ya aiko tsawawwaki a kanta daga sama, ta zama kasa mai santsi.
40. Ko ruwanta ya zama kafaffe bazaka sami ikon nema ba gareshi.
41. Ilai kuwa sai aka kewaye da ita (wato amfanin gonarsa wato aka halakar da gonar) saiya zama yana juya tafukansa (don nadama,) a kan abinda ya ciyar a cikinta, a raya ta alhali tana sarye a kan al'amudanta (shine ta fadi, inabin) kuma ya fadi kanta, yana cewa yana mana ki! Daya kace ni ban tara kowa tareda Ubangijina ba.
42. Watajama'a da zata taimake shi ba Allah ba, bata kasance a gareshi ba, (yayin halakar gonan nan,) shi kuma bai kasance zai iya taimakon kansa da kansa ba.
43. Cananka ranar alkiyama taimako ga Allah tabbataccen sarki yake, shine mafi kyakkyawan sakamako. shine mafi kyakkyawan karshe (ga muminai).

(IRIN MISALIN RAYUWAR DUNIYA)

44. Kwatanta musu sifar rayuwar duniya (halinta) kamar ruwa ne muka saukar dashi daga sama sai tsirin kasa ya cudanya saboda saukar ruwan nan, sai tsirin nan ya zama kekashasshe mar-mashasshe, iskoki suna sheke shi, (wato ma'anar kwatanta musu duniya da tsiri kyakkyawa daya kekashe ya murmushe iska ta sheke shi) Allah mai girman iko ne a kan komai.

ٱلْمَالُ وَٱلْبَنُونَ زِينَةُ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا وَٱلْبَٰقِيَٰتُ ٱلصَّٰلِحَٰتُ خَيْرٌ عِندَ
رَبِّكَ ثَوَابًا وَخَيْرٌ أَمَلًا ﴿45﴾ وَيَوْمَ نُسَيِّرُ ٱلْجِبَالَ وَتَرَى ٱلْأَرْضَ
بَارِزَةً وَحَشَرْنَٰهُمْ فَلَمْ نُغَادِرْ مِنْهُمْ أَحَدًا ﴿46﴾ وَعُرِضُوا عَلَىٰ
رَبِّكَ صَفًّا لَّقَدْ جِئْتُمُونَا كَمَا خَلَقْنَٰكُمْ أَوَّلَ مَرَّةٍۭ بَلْ زَعَمْتُمْ
أَلَّن نَّجْعَلَ لَكُم مَّوْعِدًا ﴿47﴾ وَوُضِعَ ٱلْكِتَٰبُ فَتَرَى ٱلْمُجْرِمِينَ
مُشْفِقِينَ مِمَّا فِيهِ وَيَقُولُونَ يَٰوَيْلَتَنَا مَالِ هَٰذَا ٱلْكِتَٰبِ لَا يُغَادِرُ
صَغِيرَةً وَلَا كَبِيرَةً إِلَّا أَحْصَىٰهَا وَوَجَدُوا مَا عَمِلُوا حَاضِرًا وَلَا يَظْلِمُ
رَبُّكَ أَحَدًا ﴿48﴾ وَإِذْ قُلْنَا لِلْمَلَٰٓئِكَةِ ٱسْجُدُوا لِءَادَمَ فَسَجَدُوٓا
إِلَّآ إِبْلِيسَ كَانَ مِنَ ٱلْجِنِّ فَفَسَقَ عَنْ أَمْرِ رَبِّهِۦٓ
أَفَتَتَّخِذُونَهُۥ وَذُرِّيَّتَهُۥٓ أَوْلِيَآءَ مِن دُونِي وَهُمْ لَكُمْ عَدُوٌّۢ
بِئْسَ لِلظَّٰلِمِينَ بَدَلًا ﴿49﴾ مَّآ أَشْهَدتُّهُمْ خَلْقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ وَلَا خَلْقَ أَنفُسِهِمْ وَمَا كُنتُ مُتَّخِذَ ٱلْمُضِلِّينَ عَضُدًا ﴿50﴾
وَيَوْمَ يَقُولُ نَادُوا شُرَكَآءِيَ ٱلَّذِينَ زَعَمْتُمْ فَدَعَوْهُمْ
فَلَمْ يَسْتَجِيبُوا لَهُمْ وَجَعَلْنَا بَيْنَهُم مَّوْبِقًا ﴿51﴾ وَرَءَا ٱلْمُجْرِمُونَ ٱلنَّارَ
فَظَنُّوٓا أَنَّهُم مُّوَاقِعُوهَا وَلَمْ يَجِدُوا عَنْهَا مَصْرِفًا ﴿52﴾

45. Dukiya da "ya"ya adon rayuwar duniya ne ayyuka nagargaru (zikiri ko waninsu) masu wanzuwa, sune sukafi sakamako nan ga ubangijinka, shine yafi am-fani a wajen sakamako.

(DAGA MATSAYAN RANAR ALƘIYAMA)

46. Ka ambata ranar da muke tafiyar da duwarwatsu (ga buran fuskar ƙasa ta zama kura abar shekewa, kana ganin ƙasa a bayyane (ba kome a kanta nadaga duwatsu ko waninsu) muka tara muminai da kafirai ba mubar ɗaya daga cikinsu ba.

47. Aka bujirar dasu ga ubangijinka, sahusahu, (a ce dasu) " Haƙiƙa kun zo mana kamar yadda muka halicce ku marrar farko, (daidawa,tsirara, masu loba, ana faɗa ga masu musun tashin alƙiyama) kai! ai kun riyacewa bazamu sanya muku alƙawari (na tashin alƙiyama) ba.

48. aka sanya takardar (kowane mumini a hannunsa na dama, kafiri kuma a hannunsa na hagu,) kana ganin kafirai matsorata daga abinda yake cikinsa, suna cewa, (yayin ganin abinda yake cikinsa na daga miyagun ayyuka,) "Wohoho! Kaiconmu!! Me ya sami wannan littafi baya barin ƙanƙane ko babba (na daga zunubanmu) saiya lissafe mana ita. "(Suna mana kin wannan abu, suka sami abinda suka aikata a hallare (a cikin littafinsu,) Ubangijinka baya zaluntar kowa, (Yayi uƙuba bada laifi bako ya tauye lada.)

(GARGADI DAGA UBANGIJI)

49. Ka ambata zamanin da muka faɗa ga Mala'iku "Kuyi sujada ga Annabi Adamu (mai tsira da amincin Allah, sunkuyo ba dungurawa ba,)" Sukayi sajada sai Iblis kaɗai ya kasance daga aljannu, yai fasiƙanci ga buran umarnin Ubangijinsa (bai yi sajada ba,) donme zaku ruƙe shi da zuriyarsa bani ba, alhali su magauta ne gareku, tur! musanyaga azzalumai.

50. Ban nuna musu halittar sammai da ƙassai ba, (Iblis da mutanensa,) ban nuna musu halittar kansu ba, Ni ban kasance mai riƙon masu ɓatarwa mataimaka ba, (dom me kuke bin su.)

51. Ka ambaci ranar da muke cewa, "Ku kirawo ababan tarayya dani (sune gumakanku) waɗanda kuke riya (masu ceto a gareku,) suka kira su basu amsa musu ba, muka sanya zazan jahannama a tsakaninsu (su gumakan da masu bautar.)

52. Ma'abuta laifi suka ga wuta, suka tabbatacewa haƙiƙa su, masu faɗawa ne a cikinta, basu sami maƙarɗaɗa ga buran ta ba.

(FIRGITARWA DA TSORATARWA)

رُبع

* وَلَقَدْ صَرَّفْنَا فِي هَٰذَا الْقُرْءَانِ لِلنَّاسِ مِن كُلِّ مَثَلٍ وَكَانَ الْإِنسَانُ
أَكْثَرَ شَيْءٍ جَدَلًا ﴿53﴾ وَمَا مَنَعَ النَّاسَ أَن يُؤْمِنُوا إِذْ جَاءَهُمُ الْهُدَىٰ
وَيَسْتَغْفِرُوا رَبَّهُمْ إِلَّا أَن تَأْتِيَهُمْ سُنَّةُ الْأَوَّلِينَ
أَوْ يَأْتِيَهُمُ الْعَذَابُ قِبَلًا ﴿54﴾ وَمَا نُرْسِلُ الْمُرْسَلِينَ إِلَّا مُبَشِّرِينَ
وَمُنذِرِينَ وَيُجَادِلُ الَّذِينَ كَفَرُوا بِالْبَاطِلِ لِيُدْحِضُوا بِهِ الْحَقَّ
وَاتَّخَذُوا ءَايَاتِي وَمَا أُنذِرُوا هُزُؤًا ﴿55﴾ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن ذُكِّرَ
بِـَٔايَاتِ رَبِّهِ فَأَعْرَضَ عَنْهَا وَنَسِيَ مَا قَدَّمَتْ يَدَاهُ
إِنَّا جَعَلْنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ أَكِنَّةً أَن يَفْقَهُوهُ وَفِي ءَاذَانِهِمْ
وَقْرًا وَإِن تَدْعُهُمْ إِلَى الْهُدَىٰ فَلَن يَهْتَدُوا
إِذًا أَبَدًا ﴿56﴾ وَرَبُّكَ الْغَفُورُ ذُو الرَّحْمَةِ لَوْ يُؤَاخِذُهُم
بِمَا كَسَبُوا لَعَجَّلَ لَهُمُ الْعَذَابَ بَل لَّهُم مَّوْعِدٌ لَّن يَجِدُوا
مِن دُونِهِ مَوْئِلًا ﴿57﴾ وَتِلْكَ الْقُرَىٰ أَهْلَكْنَاهُمْ لَمَّا ظَلَمُوا وَجَعَلْنَا
لِمَهْلِكِهِم مَّوْعِدًا ﴿58﴾ وَإِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِفَتَاهُ لَا أَبْرَحُ حَتَّىٰ
أَبْلُغَ مَجْمَعَ الْبَحْرَيْنِ أَوْ أَمْضِيَ حُقُبًا ﴿59﴾ فَلَمَّا بَلَغَا مَجْمَعَ
بَيْنِهِمَا نَسِيَا حُوتَهُمَا فَاتَّخَذَ سَبِيلَهُ فِي الْبَحْرِ سَرَبًا ﴿60﴾

53. Haƙiƙa mun bayyana ga mutane a cikin wannan alƙur'ani daga dukkan misali (donsu wa'azantu,) mutum (kafiri) ya kasance mafi yawan jayayya daga kowane abu .
54. Ba abinda ya hana mutanen (Makka) su bada gaskiya, zam-anin da Alƙur'ani yazo musu su nemi gafarar Ubangijinsu wai sai sunnonin mutanen farko tazo musu (Itace halakarwa, ko azabatazo musu ƙarara).
55. Barna aiko manzanni sai masu albishir (ga muminai,) masu tsoratarwa (ga kafirai,) waɗanda suka kafirta suna yin jayayya da ƙarya, (suna cewa "ƙaƙa Allah zai aiko manzo daga "yan Adam,) don rushe gaskiya dashi jidalin nasu, (wato su rushe, alƙur'ani) sun riƙi ayoyina na ƙur'ani da abinda ake basu tsoro (dashi na wuta) abin izgili .
56. Ba mafi zalunci daga wanda aka gargade shi da ayoyin Ubangijinsa ya bujire ga buranta, ya mance abinda hannunsa ta gabatar (na aikin kafirci da sabo,) mu mun sanya rufe-rufe a kan zukatansu, don kadasu fahimci alƙur'ani, mun sanya nauyi a cikin kunnuwansu, bazasu amfanu da wa'azinsa ba in kayi kiransu izuwa shiriya to, bazasu shiriyaba yayih nan har abada.
57. Ubangijinka shine mai yawan gafara mai jinƙai, dayana kama su a duniya da abinda suka aikata, dayagaggauta musu azaba (a cikinta,) ban alƙawari na garesu (shine ranar alƙiyama,) bazasu sami mafaka ba tare dashi,
58. Waɗancananka alƙaryatu mun halakar da mutanenta (wato Samudu da waninsu,) yayin da sukai kafirci, mun sanya lokaci ga halakar dasu.

(ƘISSAR ANNABI MUSA TAREDA HALLIRU ALAIHI MASSALAMU)

59. Ka ambata zamanin da Annabi Musa (dan Imrana) ya faɗa ga saurayinsa (Yusha'u dan Nuna ya kasance yana bin sa yanayi masa hidima yana karɓar ilmi daga gareshi wato ɗalibta,) "Bazan gushe ba ina tafiya har in isa matattarar kogi guda biyu, (magam a kogin Rum da kogin Fadsa daga nahiyar gabas a Ifriƙiya,) ko in wuce zamani mai tsawo (a cikin riskarsa in ya kasance mai nisa".)
60. A yayin da suka isa matattarar kogunan nan guda biyu sai suka mance kifinsu, (wato Yusha'u ya mance ya dauƙi kifi Annabi Musa alaihissalam ya mance ya tuna masa,) sai kifi ya riƙi han-yarsa a cikin kogi hanya a mike (amma ba mai wucewa ba saboda Allah ya riƙe gudun ruwa ga buran wannan kifi, sai ruwa ya yaye ga buransa, saiya zama kamar alkuki bai hadu ba, abinda yake ƙarƙashinsa yasandare.)

فَلَمَّا جَاوَزَا قَالَ لِفَتَىٰهُ ءَاتِنَا غَدَآءَنَا لَقَدْ لَقِينَا مِن سَفَرِنَا
هَٰذَا نَصَبًا ﴿61﴾ قَالَ أَرَءَيْتَ إِذْ أَوَيْنَآ إِلَى ٱلصَّخْرَةِ فَإِنِّي نَسِيتُ ٱلْحُوتَ
وَمَآ أَنسَىٰنِيهُ إِلَّا ٱلشَّيْطَٰنُ أَنْ أَذْكُرَهُۥ وَٱتَّخَذَ سَبِيلَهُۥ
فِي ٱلْبَحْرِ عَجَبًا ﴿62﴾ * قَالَ ذَٰلِكَ مَا كُنَّا نَبْغِ فَٱرْتَدَّا عَلَىٰٓ ءَاثَارِهِمَا
قَصَصًا ﴿63﴾ فَوَجَدَا عَبْدًا مِّنْ عِبَادِنَآ ءَاتَيْنَٰهُ رَحْمَةً مِّنْ عِندِنَا
وَعَلَّمْنَٰهُ مِن لَّدُنَّا عِلْمًا ﴿64﴾ قَالَ لَهُۥ مُوسَىٰ هَلْ أَتَّبِعُكَ عَلَىٰٓ أَن
تُعَلِّمَنِ مِمَّا عُلِّمْتَ رُشْدًا ﴿65﴾ قَالَ إِنَّكَ لَن تَسْتَطِيعَ مَعِيَ صَبْرًا ﴿66﴾
وَكَيْفَ تَصْبِرُ عَلَىٰ مَا لَمْ تُحِطْ بِهِۦ خُبْرًا ﴿67﴾ قَالَ سَتَجِدُنِيٓ إِن شَآءَ ٱللَّهُ
صَابِرًا وَلَآ أَعْصِي لَكَ أَمْرًا ﴿68﴾ قَالَ فَإِنِ ٱتَّبَعْتَنِي فَلَا تَسْـَٔلْنِي
عَن شَيْءٍ حَتَّىٰٓ أُحْدِثَ لَكَ مِنْهُ ذِكْرًا ﴿69﴾ فَٱنطَلَقَا
حَتَّىٰٓ إِذَا رَكِبَا فِي ٱلسَّفِينَةِ خَرَقَهَا قَالَ أَخَرَقْتَهَا لِتُغْرِقَ أَهْلَهَا
لَقَدْ جِئْتَ شَيْـًٔا إِمْرًا ﴿70﴾ قَالَ أَلَمْ أَقُلْ إِنَّكَ لَن تَسْتَطِيعَ مَعِيَ
صَبْرًا ﴿71﴾ قَالَ لَا تُؤَاخِذْنِي بِمَا نَسِيتُ وَلَا تُرْهِقْنِي مِنْ أَمْرِي
عُسْرًا ﴿72﴾ فَٱنطَلَقَا حَتَّىٰٓ إِذَا لَقِيَا غُلَٰمًا فَقَتَلَهُۥ قَالَ أَقَتَلْتَ
نَفْسًا زَكِيَّةً بِغَيْرِ نَفْسٍ لَّقَدْ جِئْتَ شَيْـًٔا نُّكْرًا ﴿73﴾

ثمن

61. A yayin da suka ƙetare (wannan wuri da tafiya, izuwa lokacin cin abincinsu na wuni na rana ta biyu sai (Annabi Musa alaihissalam) yace dayaronsa, "Kawo mana abincinmu na farkon rana, haƙiƙa mun gamu da wahala a cikin tafiyarmu wannan," (basu sami wahala ba sai bayan sun ketare gun.)
62. Yace, "Kaji ko! ka tuna a yayin da muka tattara a fa (ta wancananka wuri,) to, haƙiƙa ni na mance kifinmu, ba abinda ya mantar dani shi sai shaiɗan, ya mantar dani tina shi, ya riƙi hanyarsa. a cikin kogi abin mana ki" (Annabi Musa alaihissalam dayaronsa suna mam.aki,)
63. Annabi Musa (alaihissalam) yace "Wancananka (rashin kifi,) shine abinda muka kasance muna nema, (don alama ce bisa samun bukatarmu,)" Sai suka juyo a kan dugadugansu suna bibiyan guraba bibiya.
64. Sai suka sami bawa daga bayinmu (shine Halliru alaihissalam,) Munbashi rahama daga garemu (Annabci da walittaka,) mun sanar dashi ilimi daga garemu*.
65. Sai Annabi Musa alaihissalam yace dashi, "Shin bana bika ba a bisa ka sanar dani shiriya a bisa abinda aka sanar da kai.
66. Yace, " Haƙiƙa kai baka iya sa-mun dauriya taredani har abada.
67. "Yaya za kayi haƙuri bisa abinda baka kewaye sani dashi ba" (a cikin Hadisi wanda yagabaci wannan aya. Yace haƙiƙa ni ina bisa ilimi daga Allah dayasanar dani shi da bakasan shibakai kuma kana bisa ilimi wanda ban sanshi ba.)
68. Yace da sannu zaka same ni in Allah ya yarda mai haƙuri bazan saba maka al'amari ba (Shehu Mahalli Allah ya ƙara yarda a gareshi yace, Wannan al'adar Annabawa ce da Waliyyai bazasu amince da kansu ba kiftawar idaniya.)
69. Annabi Halliru (Alaihissalam) yace, to in ka bini, karka tambaye ni ga wani abu, saina fara maka ambato daga gareshi, Annabi Musa alaihissalam ya karɓi shardinsa don kiyaye ladabindalibi tareda malaminsa.)
70. Sai suka tafi suna tafiya a gefen kogi, har yayin da suka hau cikin komi, (waccc take tafiya dasu,) sai Annabi Halliru (Alaihissalam) ya huda ta, (shine ya cire allo biyu ko daya nata, daga jihar kogin da gatari, yayin daya isa tsatstsakin kogi, Annabi Musa alaihissalam) yace (dashi) yaya ka huda ta donka nutsar da mutanenta, haƙiƙa ka aikata abu mummuna" (amma Ance ruwan bai shiga cikin ba.)
71. Yacc, "BAnce kai haƙiƙa bazaka iya dauriya taredani ba ne."
72. Yace, kadaka riƙe ni da abinda na mance, kadaka kallafa min tsanani daga al'amarina."
73. Suka tafi (bayan fitarsu daga cikin jirgi suna tafiya a ƙasa) har yayin da suka gamu da wani yaro (wanda bai balaga ba yana wasa tare dayara, yafi su kyan fuska,) sai Annabi Halliru ya kashe shi, (ya yanka shi da wuka) "Yaya zaka kashe kai tsatstsarka (bata isa haddin taklifi ba,) ba tareda wata kai data kashe ba, haƙiƙa ka aikata aiki mummuna."

* (Ilimin Ilhama da gaibobi, Buhari ya ruwaito Hadisi cewa Annabi Musa alaihissalam ya tashi yana huɗuba a cikin Bani-Isra'ila aka tambaye shi wanene yafi sani a cikin mu-tane, sai yace, Ni, sai Allah ya zarge shi a bisa wannan, don bai mayar da ilimi izuwa gareshi ba, (bai ce Allahu-aalamu ba) sai Allah ya aiko izuwa gareshi, haƙiƙa ina da wani bawa a matattarar koguna yafi ka sani, Annabi Musa alaihissalam yace, Ya Rabbi ƙaƙa zan iya saduwa dashi, yace ka riƙi kifi tareda kai, ka sanyashi a cikin sanho, a indaka rasa kifin nan, to, shi yana nan gun, saiya ɗauki kifi Ya sanyashi a cikin sanho, sannan ya tafi, yaronsa Annabi Yusha'u alaihissalam ya tafi, tare dashi, har suka zowa fa, suka ajiye kawukansu sukayi bacci, kifi yayi tsalle a cikin sanho yafita daga ciki ya faɗa cikin kogi, ya kama hanyarsa kai"tsaye a cikin kogi, Allah ya kame masa gudun ruwa, ya zama a kansa kamar taga, a yayin daya farka sai abokinsa ya mance ya bashi labari da kifi, sai suka hau tafiya, darensu da ranarsu, har idan suka kasance daga safiya sai Annabi Musa alaihissalam yace da Annabi Yusha'u alaihissalam bamu abincinmu, Har izuwa faɗinsa; ya riki hanyarsa cikin kogi". Sai manzon Allah yace : "Wato ya kasance hanyaga kifi. Mana ki ga Annabi Musa da sawrayinsa alaihimussalamu.

حزب

۞ قَالَ أَلَمْ أَقُل لَّكَ إِنَّكَ لَن تَسْتَطِيعَ مَعِيَ صَبْرًا ﴿74﴾ قَالَ إِن سَأَلْتُكَ
عَن شَيْءٍ بَعْدَهَا فَلَا تُصَاحِبْنِي قَدْ بَلَغْتَ مِن لَّدُنِي عُذْرًا ﴿75﴾
فَانطَلَقَا حَتَّىٰ إِذَا أَتَيَا أَهْلَ قَرْيَةٍ اسْتَطْعَمَا أَهْلَهَا فَأَبَوْا أَن يُضَيِّفُوهُمَا
فَوَجَدَا فِيهَا جِدَارًا يُرِيدُ أَن يَنقَضَّ فَأَقَامَهُ قَالَ لَوْ شِئْتَ
لَتَخِذْتَ عَلَيْهِ أَجْرًا ﴿76﴾ قَالَ هَٰذَا فِرَاقُ بَيْنِي وَبَيْنِكَ سَأُنَبِّئُكَ
بِتَأْوِيلِ مَا لَمْ تَسْتَطِع عَّلَيْهِ صَبْرًا ﴿77﴾ أَمَّا السَّفِينَةُ فَكَانَتْ لِمَسَاكِينَ
يَعْمَلُونَ فِي الْبَحْرِ فَأَرَدتُّ أَنْ أَعِيبَهَا وَكَانَ وَرَاءَهُم مَّلِكٌ
يَأْخُذُ كُلَّ سَفِينَةٍ غَصْبًا ﴿78﴾ وَأَمَّا الْغُلَامُ فَكَانَ أَبَوَاهُ مُؤْمِنَيْنِ فَخَشِينَا
أَن يُرْهِقَهُمَا طُغْيَانًا وَكُفْرًا ﴿79﴾ فَأَرَدْنَا أَن يُبَدِّلَهُمَا رَبُّهُمَا
خَيْرًا مِّنْهُ زَكَاةً وَأَقْرَبَ رُحُمًا ﴿80﴾ وَأَمَّا الْجِدَارُ فَكَانَ
لِغُلَامَيْنِ يَتِيمَيْنِ فِي الْمَدِينَةِ وَكَانَ تَحْتَهُ كَنزٌ لَّهُمَا
وَكَانَ أَبُوهُمَا صَالِحًا فَأَرَادَ رَبُّكَ أَن يَبْلُغَا أَشُدَّهُمَا
وَيَسْتَخْرِجَا كَنزَهُمَا رَحْمَةً مِّن رَّبِّكَ وَمَا فَعَلْتُهُ عَنْ أَمْرِي
ذَٰلِكَ تَأْوِيلُ مَا لَمْ تَسْطِع عَّلَيْهِ صَبْرًا ﴿81﴾ ۞ وَيَسْأَلُونَكَ
عَن ذِي الْقَرْنَيْنِ قُلْ سَأَتْلُو عَلَيْكُم مِّنْهُ ذِكْرًا ﴿82﴾

ثمن

74. Sai yace, "BAnce maka haƙiƙca kai bazaka sami ikon dauriya taredani ba ne?"

75. Yace, "In na kuma tambayarka bayanta ga wani abu bayan wannan marra to, kadaka abuce ni, haƙiƙa ka isa hanzari daga gare ni."

76. Suka tafi har lokacin da suka zowa mutanen wata alƙarya, (da ake ce mata Anɗakiya) sai suka nemi liyafa daga mutanenta, sai suka ƙi suyi musu liyafar, sai suka sami garu a cikinta mai daukakar kamu dari,) yana nufin ya silmanyo, sai Halliru ya daidaita shi da hannunsa, sai Annabi Musa yace (dashi) daka ga dama daka riƙi lada a kansa, (tun da suka ƙi suyi mana liyafa tareda bukatarmu izuwa abinci.)

77. Sai Halliru yace dashi, "Wannan shine rabuwa tsakanina da kai, da sannu (gaban rabuwarmu) zan baka labarin fassarar abinda baka iya daurewa a kansa ba.

78. "Amma wannan komi ta ka-sance ga miskinai (guda goma ne,) dasuke aiki a cikin kogi (wato kodago,) na nufi in laifantata, akwai wani sarki (kafiri) a gabansu (a yanzu a bayansu in sun koma) yana ƙwace dukkan komi (lafiyayya) don ƙwace.

79. "Amma yaron nan kuwa, iyay-ensa sun kasance muminai mukaji tsoron ya lazunta musu shisshigi da kafirci (saboda Muslim yace, an halicci wannan yaro kafiri daya rayu daya mai dasu kafirai saboda kaunar dasuke masa.)

80. Muka nufi Ubangijinsu ya musanya musu mafifici daga gareshi a nagartada taƙawa mafi ku sancinsu jinƙai (saboda bin iyaye. Ubangiji ya musanya musu dayarinya ta auri Annabi ta haifi Annabi, Allah ya shiryi al'umma dashi).

81. "Amma garu kuwa, ya kasance ne na yara guda biyu marayu, a cikin garin akwai taska tasu a ƙarƙashinsa (binnanniyar dukiya ta zinare da azurfa [1] Ubansu ya kasance managarci [2] aka kiyaye su saboda albarkar uban nan nasu, a cikin kawu-kansu da dukiyoyinsu [3] to, Ubangijinka yanufi su isa ganiyar shiriyarsu, su fitar da taskarsu. Don jinkai daga ubangijinka, ban aikata abin nan da aka ambata na keta jirgi da kashe yaro da daidaita gam da karanbanina ba, saida Ilhama daga Ubangiji. Wannan shine fassarar abinda. (ƘISSAR ZULƘARNAINI)


82. Yahudawa suna tambayarka ga Zulƙarnaini [4] Cene (da sannu) "zan ƙissanta muku a gareku labari nadaga halinsa".

1) Ance allo ne na zinare an rubuta a daya baryar tasa guda biyu bayan Bismilla, nayi mana ki ga wanda ya bada gaskiya da Raddara, yaya yake baKin ciki. Nayi ma-maki ga wanda ya bada gaskiya da arziki yaya yake wahala, nayi mana ki ga wan- daya bada gaskiya da mutuwa yaya yake farinciki, nayi mana ki ga wanda ya bada gaskiya da hisabi yaya yake rabkana, nayi mana ki ga wanda yasan duniya da juy-awarta ƙaƙa yake nutsuwa izuwa gareta, LA'ILAHA ILLALLAHU, MUHAMMA-DUR RASULULLAHI-. Adaya barin an rubota Anallahu la ilaha illa ana wahadi la sharikali na halicci hairi da sharri madalla ga wandana halicce shi saboda alheri na gudanar dashi a bisa hannusa. 2) Ubansu shine na bakwai ko na goma sunansa Kashihu-(Sawii). 3) Anan Allah yanuna albarkatar wani tana shafar wani, Allah ya sa albarkar iyayen mu da Shehunnanmu ta shafe mu Amin-(Sawii) 4) (Zulƙarnaini) sunansa "ASKANDARU" ba Annbi bane waliyyine baƙarfata shine ya gina Askandariyyaya ambacetada Askandariyya.

إِنَّا مَكَّنَّا لَهُۥ فِي الْأَرْضِ وَءَاتَيْنَٰهُ مِن كُلِّ شَيْءٍ سَبَبًا فَأَتْبَعَ سَبَبًا
حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ مَغْرِبَ الشَّمْسِ وَجَدَهَا تَغْرُبُ فِي عَيْنٍ حَمِئَةٍ
وَوَجَدَ عِندَهَا قَوْمًا ﴿83﴾ قُلْنَا يَٰذَا الْقَرْنَيْنِ إِمَّا أَن تُعَذِّبَ وَإِمَّا أَن
تَتَّخِذَ فِيهِمْ حُسْنًا ﴿84﴾ قَالَ أَمَّا مَن ظَلَمَ فَسَوْفَ نُعَذِّبُهُۥ
ثُمَّ يُرَدُّ إِلَىٰ رَبِّهِۦ فَيُعَذِّبُهُۥ عَذَابًا نُّكْرًا ﴿85﴾ وَأَمَّا مَنْ ءَامَنَ وَعَمِلَ صَالِحًا
فَلَهُۥ جَزَآءُ الْحُسْنَىٰ وَسَنَقُولُ لَهُۥ مِنْ أَمْرِنَا يُسْرًا ﴿86﴾ ثُمَّ اتَّبَعَ سَبَبًا
حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ مَطْلِعَ الشَّمْسِ وَجَدَهَا تَطْلُعُ عَلَىٰ قَوْمٍ لَّمْ نَجْعَل لَّهُم مِّن
دُونِهَا سِتْرًا ﴿87﴾ كَذَٰلِكَ وَقَدْ أَحَطْنَا بِمَا لَدَيْهِ خُبْرًا ﴿88﴾ ثُمَّ اتَّبَعَ سَبَبًا
حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ بَيْنَ السُّدَّيْنِ وَجَدَ مِن دُونِهِمَا قَوْمًا لَّا يَكَادُونَ
يَفْقَهُونَ قَوْلًا ﴿89﴾ قَالُوا يَٰذَا الْقَرْنَيْنِ إِنَّ يَاجُوجَ وَمَاجُوجَ مُفْسِدُونَ
فِي الْأَرْضِ فَهَلْ نَجْعَلُ لَكَ خَرْجًا عَلَىٰٓ أَن تَجْعَلَ بَيْنَنَا وَبَيْنَهُمْ سَدًّا ﴿90﴾
قَالَ مَا مَكَّنِّي فِيهِ رَبِّي خَيْرٌ فَأَعِينُونِي بِقُوَّةٍ أَجْعَلْ بَيْنَكُمْ وَبَيْنَهُمْ رَدْمًا ﴿91﴾
ءَاتُونِي زُبَرَ الْحَدِيدِ حَتَّىٰٓ إِذَا سَاوَىٰ بَيْنَ الصَّدَفَيْنِ قَالَ انفُخُوا
حَتَّىٰٓ إِذَا جَعَلَهُۥ نَارًا قَالَ ءَاتُونِي أُفْرِغْ عَلَيْهِ قِطْرًا ﴿92﴾
فَمَا اسْطَاعُوا أَن يَظْهَرُوهُ وَمَا اسْتَطَاعُوا لَهُۥ نَقْبًا ﴿93﴾

83. Haƙiƙa mu mun kafa shi a cikin ƙasa (da horewar tafiya a cikinta,) Munbashi iko daga kowane abu (da yake buƙata a gareshi.)
84. To, saiya shiga hanya wajen yamma har lokacin daya isa mafaɗar rana, saiya sami rana tana faɗuwa cikin idaniya ta bakin taɓo, (a ganin ido, amma a haƙiƙa bazata faɗi a cikinta ba saboda ita rana tafi duniya girma.) Ya sami mutane nan ga wannan idaniya (kafirai,) mukace "Ya Zulƙarnaini, (wato mukayi masa ilhami,) imma ka azabci mutanen nan da kisa, ko kuma ka riƙi kyakkyawa daga garesu (shine ribacewa.)
85. Yace, "Amma wanda yayi zalunci, (yayi shirka,) dasannu zamuyi masa azaba (da kisa,) sannan mu mayar dashi izuwa ubangijinsa yayi masa azaba, azaba mummuna (a cikin wuta.)
86. "Amma wanda yagasgata, yayi aiki nagari to, yana da sakamako na aljanna da sannu zamu faɗa masa sauki daga al'amarinmu".
87. Sannan ya shirya tafiya katanin gabas harya isa mahudar rana, ya sameta tana hudowa ga mutane, (wato Ama,) waɗanda bamu sanya sittira garesu koma bayanta ba, (a cikin rami suke saboda ƙasarsu bata ginuwa.)
88. Al'amarin kamar yadda muka faɗa yake, haƙiƙa mun kewaye sani da abinda yake gareshi na daga runduna da salolin yaƙi da waninsu.
89. Sannan ya shirya tafiya har lokacin daya isa tsakanin toshiya guda biyu, (duwatsune guda biyu a makurar garuruwan turkawa, dashi askandaru ya toshe abinda yake tsakaninsu,) saiya sami waɗansu mutane koma bayansu, (wato gabansu,) basa kusa su fahinci magana saida ƙyar.
90. Sai sukace "Ya Zulƙarnaini, haƙiƙa Yajuju da Majuju masu barnane a bayan ƙasa, (ƙabilune guda biyu) shin barna sanya maka lada bane a bisa ka sanya toshiya tsakaninmu dasu (yadda bazasu iya saduwa izuwa garemu ba?").
91. Yace abinda Ubangijina ya bani (na dukiya da waninsa,) yafi ladanku) wanda zaku sanya gareni, zanyi wannan toshiya gareku don neman sakamakon Allah,) to, ku taimakeni da ƙarfi (ga dukkan abinda na nemeshi gareku) na sanya ƙaƙƙarfan shamaki tsakaninku dasu (wato na sanya dangarama.)
92. Kubani gumaguman baƙin ƙarfe, (a bisa gwargwadon dutse wacce ake gani da ita, ya sanya gawayi da ƙirare a tsakaninta,) hardai a lokacin daya daidaita tsakanin gyaffan duwarwatsun nan guda biyu tsakanin waɗannan duwatsu guda biyu tafiyar kwana goma sha biyu da rabin kwana, Kamar da sawi yafaɗa (da gini, ya girka ziga-zigai da wuta daura da wancananka,) sai yace ku busa, (suka busa,) har lokacin daya maida baƙin ƙarfennan wuta, sai yace ku kawomin narkakkiyar tagulla, in kwararata a kansa, (saiya kwarara narkakkiyarta a kan baƙin ƙarfen nan, ya shiga tsakanin guma-guman nan ya zama abu ɗaya.)
93. Bazasu sami damarsu hau kansa ba (saboda ɗaukakar[1] gininsa da santsinsa) bazasu sami damar busashi ba (saboda taurinsa da kaurinsa.)

1) Daukakarsa yakai zira'i maitan



قَالَ هَٰذَا رَحْمَةٌ مِّن رَّبِّيٓ فَإِذَا جَآءَ وَعْدُ رَبِّي جَعَلَهُۥ دَكّاً وَكَانَ وَعْدُ
رَبِّي حَقّاً ﴿94﴾ * وَتَرَكْنَا بَعْضَهُمْ يَوْمَئِذٍ يَمُوجُ فِي بَعْضٍ وَنُفِخَ فِي الصُّورِ
فَجَمَعْنَٰهُمْ جَمْعاً ﴿95﴾ وَعَرَضْنَا جَهَنَّمَ يَوْمَئِذٍ لِّلْكَٰفِرِينَ عَرْضاً ﴿96﴾
الَّذِينَ كَانَتْ أَعْيُنُهُمْ فِي غِطَآءٍ عَن ذِكْرِي وَكَانُواْ لَا يَسْتَطِيعُونَ سَمْعاً ﴿97﴾
أَفَحَسِبَ الَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَن يَتَّخِذُواْ عِبَادِي مِن دُونِيَ أَوْلِيَآءَ
إِنَّا أَعْتَدْنَا جَهَنَّمَ لِلْكَٰفِرِينَ نُزُلاً ﴿98﴾ قُلْ هَلْ نُنَبِّئُكُم بِالْأَخْسَرِينَ
أَعْمَٰلاً الَّذِينَ ضَلَّ سَعْيُهُمْ فِي الْحَيَوٰةِ الدُّنْيَا وَهُمْ يَحْسِبُونَ أَنَّهُمْ
يُحْسِنُونَ صُنْعاً ﴿99﴾ أُوْلَٰٓئِكَ الَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمْ وَلِقَآئِهِۦ فَحَبِطَتْ
أَعْمَٰلُهُمْ فَلَا نُقِيمُ لَهُمْ يَوْمَ الْقِيَٰمَةِ وَزْناً ﴿100﴾ ذَٰلِكَ جَزَآؤُهُمْ جَهَنَّمُ
بِمَا كَفَرُواْ وَاتَّخَذُوٓاْ ءَايَٰتِي وَرُسُلِي هُزُؤاً ﴿101﴾ إِنَّ الَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ
الصَّٰلِحَٰتِ كَانَتْ لَهُمْ جَنَّٰتُ الْفِرْدَوْسِ نُزُلاً ﴿102﴾ خَٰلِدِينَ فِيهَا لَا يَبْغُونَ
عَنْهَا حِوَلاً ﴿103﴾ قُل لَّوْ كَانَ الْبَحْرُ مِدَاداً لِّكَلِمَٰتِ رَبِّي لَنَفِدَ الْبَحْرُ
قَبْلَ أَن تَنفَدَ كَلِمَٰتُ رَبِّي وَلَوْ جِئْنَا بِمِثْلِهِۦ مَدَداً ﴿104﴾ قُلْ إِنَّمَآ أَنَا بَشَرٌ
مِّثْلُكُمْ يُوحَىٰٓ إِلَيَّ أَنَّمَآ إِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَٰحِدٌ فَمَن كَانَ يَرْجُواْ لِقَآءَ
رَبِّهِۦ فَلْيَعْمَلْ عَمَلاً صَٰلِحاً وَلَا يُشْرِكْ بِعِبَادَةِ رَبِّهِۦٓ أَحَداً ﴿105﴾

94. Zulƙarnaini yace, "Wannan (to-shiya wato bani iko a kai,) rahamace daga Ubangijina, (don shine mai hanasu fitowa,) idan alƙawarin ubangijina yazo (da fitarsu, na kusanci da tashin alƙiyama,) sai Ubangiji ya maidashi dandaƙaƙƙe alƙawarin Ubangiji na da fitarsu da waninsa ya tabbata gaskiya.

(AḰIBAR KAFIRCI RANAR ALḰIYAMA)

95. Mukabar ba'alinsu a wannan rana yana kunzuma a cikin ba'ali, akayi busa a cikin ƙaho don tashin alƙiyama, muka tara talikai a wuri ɗaya a ranar alƙiyama tarawa.
96. Muka kusanto jahannama ga kafirai kusantowa.
97. Waɗanda idandunansu suka ka sance a cikin dimɗewa ga buran ambatona, Alƙur'ani, su makafine (bazasu shiriya dashi ba), sun kasance basu damu dajin Alƙur'ani daga Manzon Allah mai tsira da amincin Allah don tsananin gaba dashi.
98. Shin yanzu waɗanda suka kafirta sa zacisu riƙi bayina annabi Isa da Annabi Uzairu Alaihi-massalamu su riƙesu ubangiji bani ba, haƙiƙa mun tanadi jahannama garan baƙi ga kafirai.
99. Cene shin bana baku labari da mafi tabewar ayyuka bane, sune waɗanda aikinsu ya lalace a rayuwar duniya, alhalisu suna zaton haƙiƙa su masu kyakkyawan ayyukanc.
100. Waɗancananka sune waɗanda suka kafirtada ayoyin ubangijinsu, da gamuwa dashi, sai ayyukansu suka lalace. Bazamu sanya musu alƙadari ba ranar alƙiyama.
101. Wancananka bacin ayyuka da waninsa sakamakonsu a kansa jahannama saboda sunyi kafirci sun riƙi ayoyina da Manzannina abin izgili dasu.

(AḰIBAR IMANI DA AIKI NAGARI)

102. Haƙiƙa waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiyuka nagargaru, aljannatai sune Firdausu sun kasance garan bakinsu.
103. Masu dauwama a cikinta bazasu nemi juyawa ga buranta ba izuwa waninta.

(CIKAKKEN SANIN UBANGIJI DA KEWAYEWARSA DA KOMAI)

104. Cene da ruwan kogi ya kasance tawada ga kalmomin Ubangijina masu shiryarwa a kan hikimominsa da mana kansa da kogin ya ƙare a cikin rubutata, bada kalmomin Ubangiji sun ƙareba, koda zamuzoda misalinsa ƙari.
105. Cene dahir ni mutumne kamarku kawai ake aikowa izuwa gareni, cewa Ubangijinku, ubangijine guda ɗaya kawai, to, duk wanda ya kasance yana ƙaunar saduwa da ubangijinsa a tashi daga kushewa da sakamako, to, yayi aiki nagari, yayi Ihlasi (wato tsarkake niyya) kada yatara kowa cikin ibadar ubangijinsa, yayi don Allah shi kaɗai.

19 سورة مريم مكية
وهي ثمان وتسعون آية 98

ثمن

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

كٓهيعٓصٓ ذِكْرُ رَحْمَتِ رَبِّكَ عَبْدَهُۥ زَكَرِيَّآءَ 1
إِذْ نَادَىٰ رَبَّهُۥ نِدَآءً خَفِيًّا 2 قَالَ رَبِّ إِنِّي وَهَنَ الْعَظْمُ مِنِّي
وَاشْتَعَلَ الرَّأْسُ شَيْبًا وَلَمْ أَكُنۢ بِدُعَآئِكَ رَبِّ شَقِيًّا 3 وَإِنِّي
خِفْتُ الْمَوَالِيَ مِن وَرَآءِي وَكَانَتِ امْرَأَتِي عَاقِرًا فَهَبْ لِي
مِن لَّدُنكَ وَلِيًّا 4 يَرِثُنِي وَيَرِثُ مِنْ ءَالِ يَعْقُوبَ
وَاجْعَلْهُ رَبِّ رَضِيًّا 5 يَٰزَكَرِيَّآءُ إِنَّا نُبَشِّرُكَ بِغُلَٰمٍ اسْمُهُۥ يَحْيَىٰ
لَمْ نَجْعَل لَّهُۥ مِن قَبْلُ سَمِيًّا 6 قَالَ رَبِّ أَنَّىٰ يَكُونُ
لِي غُلَٰمٌ وَكَانَتِ امْرَأَتِي عَاقِرًا وَقَدْ بَلَغْتُ مِنَ الْكِبَرِ
عِتِيًّا 7 قَالَ كَذَٰلِكَ قَالَ رَبُّكَ هُوَ عَلَيَّ هَيِّنٌ
وَقَدْ خَلَقْتُكَ مِن قَبْلُ وَلَمْ تَكُ شَيْـًٔا 8 قَالَ رَبِّ اجْعَل لِّي ءَايَةً
قَالَ ءَايَتُكَ أَلَّا تُكَلِّمَ النَّاسَ ثَلَٰثَ لَيَالٍ سَوِيًّا 9 فَخَرَجَ عَلَىٰ قَوْمِهِۦ
مِنَ الْمِحْرَابِ فَأَوْحَىٰ إِلَيْهِمْ أَن سَبِّحُوا بُكْرَةً وَعَشِيًّا 10

Suratu Maryamu
(MAI tsira da Amincin Allah)Su Tabbata Agareta)
A Makka Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Casa'in Da Tara (99)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan-talikai a duniya gaba ɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

'Wannan sura tana tabbatar da Tauhidi wato kaɗaita allah, da kore shariki da ɗa ga buransa, da tabbatar da tashin alƙiyama, kuma ta sanya ƙissoshi sune tushen wannan da kuma ambaton tashin matsayan ranar Alƙiyama da bincike bincike ga masu musun tashin alƙiyama ".

(ƘISSAR ANNABI ZAKARIYA'U TSIRAN ALLAH DA AMINCINSA YA TABBATA GARESHI)

1. K.H.Y.'A.S. (Allah ne masanin abin nufi da wannan,) Ambaton rahamar Ubangijinka, bawansa Annabi Zakariya'u (mai tsira da amincin Allah.)
2. Zamanin daya kira Ubangijinsa kira ɓoyayye, (a asirce a tsakar dare, domin shine mafi gaggawa ga amsawa.)
3. Yace "Ubangijina haƙiƙa ni dukkan ƙashin da yake daga gareni ya raunana, kaina ya huro da furfura, (wato ya burwatse da furfura, ni ina nufin in roƙeka,) ban kasance taɓaɓɓe ga roƙonka ba, (a cikin abinda yagabata, kadaka taɓar dani cikin abinda zaizo.)
4. Haƙiƙa ninaji tsoron "ya"yan dangina bayan mutuwata, (ina gudun kadasu tozarta addini, tamfar dana gani cikin Bani-Isra'ila nadaga canja addini,) matata ta kasance bakarara, (ɓata haihuwa) to, bani ɗa daga gareka.
5. Da yake gadona, yake gado daga "ya"yan Yaƙuba (ƙaƙana, yake gadon ilimi da annabci) ka sanyashi yardajje (daga gareka".)
6. (Ubangiji ya faɗa a cikin amsa roƙonsa na ɗa wanda jinkansa ya tabbata dashi.) "Ya Zakariya'u haƙiƙa mu munayi maka albishir dayaro (da zaiyi gado kamar yadda kayi bara,) sunansa Yahaya, bamu sanya masa takwara ba gabansa".
7. Yace, "Ubangiji, ƙaƙa yaro zai kasance daga gareni alhalin matata takasance bakarara, ni kuma na isa shekarun ruɗewa, (na girman shekaru, shekara ɗari da ishirin (120) matata kuwa shekara casa'in da takwas (98)."
8. Yace "(al'amarin) haka yake (na halittar da daga gareku,)" Ubangijinka yace, "Shi sassauƙane a gareni, (in mayar maka da ƙarfin tarawa in buɗe mahaifar matarka don ɗanfarar ciki,) haƙiƙa na halicce ka tun da can, baka kasance komai ba (saboda bayyana wannan ikon Allah mai girma, Allah ya kimsa masa wannan tambaya don a amsa masa da abinda ya shiryar kansa. Yayin da ransa tayi bege izuwa gaggawan abinda akayi masa albishir dashi.)
9. Sai yace, "Ubangijina sanya min alama bisa cikin matata" sai yace "Alamarka a gareshi, ka rasa iya zance da mutane kwana uku daidai."
10. yafita ga mutanensa daga masallaci, (sun kasance suna sauraronsa donsu buɗeshi da umarninsa, suyi salla a cikinsa bisa al'adar da suka saba,) sai yayi musu ishara, kuyi salla safiya dayammaci (kamar yadda aka saba, to, yasani saboda hanuwarsa da zance dasu, cewa mata tasa tayi cikin annabi Yahaya, bayan haihuwarsa da shekara biyu sai Ubangiji yace dashi;)

يَٰيَحْيَىٰ خُذِ الْكِتَٰبَ بِقُوَّةٖ وَءَاتَيْنَٰهُ الْحُكْمَ صَبِيّاٗ ﴿11﴾ وَحَنَاناٗ
مِّن لَّدُنَّا وَزَكَوٰةٗ وَكَانَ تَقِيّاٗ ﴿12﴾ وَبَرّاَۢ بِوَٰلِدَيْهِ وَلَمْ
يَكُن جَبَّاراً عَصِيّاٗ ﴿13﴾ وَسَلَٰمٌ عَلَيْهِ يَوْمَ وُلِدَ وَيَوْمَ
يَمُوتُ وَيَوْمَ يُبْعَثُ حَيّاٗ ﴿14﴾ وَاذْكُرْ فِي الْكِتَٰبِ مَرْيَمَ
إِذِ انتَبَذَتْ مِنْ أَهْلِهَا مَكَاناٗ شَرْقِيّاٗ ﴿15﴾ فَاتَّخَذَتْ مِن
دُونِهِمْ حِجَاباٗ فَأَرْسَلْنَا إِلَيْهَا رُوحَنَا فَتَمَثَّلَ لَهَا بَشَراً
سَوِيّاٗ ﴿16﴾ قَالَتْ إِنِّيَ أَعُوذُ بِالرَّحْمَٰنِ مِنكَ إِن كُنتَ تَقِيّاٗ ﴿17﴾
قَالَ إِنَّمَا أَنَا رَسُولُ رَبِّكِ لِأَهَبَ لَكِ غُلَٰماً زَكِيّاٗ ﴿18﴾
قَالَتْ أَنَّىٰ يَكُونُ لِي غُلَٰمٌ وَلَمْ يَمْسَسْنِي بَشَرٌ وَلَمْ أَكُ بَغِيّاٗ ﴿19﴾
قَالَ كَذَٰلِكِ قَالَ رَبُّكِ هُوَ عَلَيَّ هَيِّنٌ وَلِنَجْعَلَهُ ءَايَةٗ
لِّلنَّاسِ وَرَحْمَةٗ مِّنَّا وَكَانَ أَمْراٗ مَّقْضِيّاٗ ﴿20﴾ ۞ فَحَمَلَتْهُ فَانتَبَذَتْ ربع
بِهِۦ مَكَاناٗ قَصِيّاٗ ﴿21﴾ فَأَجَآءَهَا الْمَخَاضُ إِلَىٰ جِذْعِ النَّخْلَةِ قَالَتْ
يَٰلَيْتَنِي مِتُّ قَبْلَ هَٰذَا وَكُنتُ نَسْياٗ مَّنسِيّاٗ ﴿22﴾ فَنَادَىٰهَا مِن
تَحْتِهَا أَلَّا تَحْزَنِي قَدْ جَعَلَ رَبُّكِ تَحْتَكِ سَرِيّاٗ ﴿23﴾ وَهُزِّي
إِلَيْكِ بِجِذْعِ النَّخْلَةِ تَسَّٰقَطْ عَلَيْكِ رُطَباٗ جَنِيّاٗ ﴿24﴾

(ƘISSAR YAHAYA MAI TSIRA DA AMINCIN ALLAH, DA KASANCEWARSA MISALI GA KOWANE SAURAYI A CIKIN TSORON ALLAH DA BIN IYAYE DA SAURANSU)

11. Ya Yahaya riƙi Attaura da ƙarfi (wato yana dan shekara uku aka bashi Annabci,) Munbashi Annabci yana ɗan ƙanƙanin yaro (yana dan shekara uku.)
12. Mun sanyashi rahama (ga mutane) daga garemu, Mun sanyashi sadaka a garesu, ya kasance mai tsoron Allah (Ance bai taɓa aikata kuskure ba, bai taɓa ruwaita aikin ashsha ba.)
13. Ya sanyashi mai biyayya ga iyayensa bai kasance jabberi mai sabon ubangijinsa ba.
14. Gaisuwa (daga garemu watojinjina,) tana gareshi ranar da aka haifeshi da ranar dazai mutu da ranar daza a tasheshi yana rayayye, (a cikin waɗannan kwanuka masu firgitarwa, wacce zai ga abinda bai taɓa ganiba a cikinta, to, shi amintacce ne a cikinta.)

"ƘISSAR HAIHUWAR ANNABI ISA DAN SAYYADATUNA MARYAMU, TSIRAN ALLAH YA TABBATA GARESU. TA ƘUNSHI TSARKAKAR TADA KAMUN TADA DAUKAKAR DAN GANTA KARTADA TSANANIN BAUTAR UBANGIJINTA, WATO ALLAH YASANYA TA MISALI GA MATAYE SU KWAI KWAYE TA KAMAR DAYA SA DANTA MISALI GA MAZAJE."

15. Ka ambaci labarin Sayyadatuna Maryamu a cikin Alƙur'ani zamanin data janye a wani wuri katarnin wuri daga gabashin gidan
16. To, saita saki shamaki daga komabayansu, dominta duba kwarkwata, a kanta ko a tufafinta, ko tayi wanka daga al'ada, muka aiko Mala'ika Jibrilu zuwa gareta, saiya surantu gareta, yana ɗan Adam madaidaicin halitta.
17. Tace " Haƙiƙani, ina neman tsari da Ubangiji mai yawan rahama daga gareka, in ka kasance mai tsoron Allah" (ka hawaye ni saboda tsoronsa.)
18. Yace, "Ni dai kawai jakadan Ubangijinki ne izuwa gareki donya baki yaro mai tsarki da Annabci.
19. Saltace, "Yaya ɗa zai samu gareni, alhali wani mutum bai taɓeni bada aure, ban kuma kasance mazinaciya ba.
20. Sai yace, "Al'amarin ai haka yake, (na halittar ɗa ba tareda uba ba,) Ubangijinki yace, shi mai sauƙine gareni, (shine Jibrilu yai busa a cikinki da umarnina, kisami cikinsa, kuma) donmu sanyashi mana ki ga mutane, kuma rahama daga garemu, (ga wanda yaba gaskiya dashi,) wannan halittar nan tasa, ya kasance al'amari abin hukunci (dashi a cikin sanina.) (Sai Mala'ika Jibrilu yayi busa a cikin aljihun rigarta, saitayi hasashe da ciki, abin surantawa a mahaifarta,)
21. To, saitayi cikinsa, saita nufi guri manisanci dashi.
22. Sai naƙuda takaita izuwa kututturen dabinuwa (donta dogara a kansa saita haihu, da haihuwa dasurantuwar, da cikin ya auku a cikin sa'a ɗaya,) saitace, ya dakace ni na mutu gaban wannan al'amari na kasance abin bari abin mancewa".
23. Sai Mala'ika Jibrilu ya kirawota daga ƙarƙashinta (ya kasanc.e a ƙasa ne daga gareta,) "Kada kiyi baƙin ciki, haƙiƙa Ubangijinki yasanya ruwan ƙorama a ƙarƙashin ki, (da can kuwa ya yanke.)
24. Ki girgiza kututturen dabino izuwa gareki dabinuwar (ta kasance ƙeƙashashshiya,) ta zuzzuba a gareki, lubiya abin ɗasa.

فَكُلِي وَاشْرَبِي وَقَرِّي عَيْنًا فَإِمَّا تَرَيِنَّ مِنَ الْبَشَرِ أَحَدًا
فَقُولِي إِنِّي نَذَرْتُ لِلرَّحْمَٰنِ صَوْمًا فَلَنْ أُكَلِّمَ الْيَوْمَ إِنسِيًّا ﴿25﴾
فَأَتَتْ بِهِۦ قَوْمَهَا تَحْمِلُهُۥ قَالُوا يَٰمَرْيَمُ لَقَدْ جِئْتِ شَيْـًٔا
فَرِيًّا ﴿26﴾ يَٰأُخْتَ هَٰرُونَ مَا كَانَ أَبُوكِ امْرَأَ سَوْءٍ
وَمَا كَانَتْ أُمُّكِ بَغِيًّا ﴿27﴾ فَأَشَارَتْ إِلَيْهِ قَالُوا كَيْفَ نُكَلِّمُ مَن
كَانَ فِي الْمَهْدِ صَبِيًّا ﴿28﴾ قَالَ إِنِّي عَبْدُ اللَّهِ ءَاتَىٰنِيَ الْكِتَٰبَ
وَجَعَلَنِي نَبِيًّا ﴿29﴾ وَجَعَلَنِي مُبَارَكًا أَيْنَ مَا كُنتُ وَأَوْصَٰنِي
بِالصَّلَوٰةِ وَالزَّكَوٰةِ مَا دُمْتُ حَيًّا ﴿30﴾ وَبَرًّا بِوَٰلِدَتِي وَلَمْ
يَجْعَلْنِي جَبَّارًا شَقِيًّا ﴿31﴾ وَالسَّلَٰمُ عَلَيَّ يَوْمَ وُلِدتُّ وَيَوْمَ أَمُوتُ
وَيَوْمَ أُبْعَثُ حَيًّا ﴿32﴾ ذَٰلِكَ عِيسَى ابْنُ مَرْيَمَ قَوْلُ الْحَقِّ الَّذِي فِيهِ
يَمْتَرُونَ ﴿33﴾ مَا كَانَ لِلَّهِ أَن يَتَّخِذَ مِن وَلَدٍ سُبْحَٰنَهُۥ إِذَا قَضَىٰ
أَمْرًا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ﴿34﴾ وَأَنَّ اللَّهَ رَبِّي وَرَبُّكُمْ
فَاعْبُدُوهُ هَٰذَا صِرَٰطٌ مُّسْتَقِيمٌ ﴿35﴾ فَاخْتَلَفَ الْأَحْزَابُ مِنۢ بَيْنِهِمْ
فَوَيْلٌ لِّلَّذِينَ كَفَرُوا مِن مَّشْهَدِ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿36﴾ أَسْمِعْ بِهِمْ وَأَبْصِرْ
يَوْمَ يَأْتُونَنَا لَٰكِنِ الظَّٰلِمُونَ الْيَوْمَ فِي ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿37﴾

25. To, sai kici (daga lubiyar nan,) kisha (daga ruwan nan mai kwarara,) ki sanyaya idaniya, (wato idanunki tayi sanyi da wannan ɗa, karkisa kwaɗayi izuwa waninsa,) idan kinka ga wani daga cikin 'yan Adam (ya tambaye ki ga wannan da naki,) to, cene haƙiƙa ni nayi alwashin azumin magana saboda ubangiji mai yawan jinƙai, (bazanyi zance da wani bil-Adama ba a yau.)
26. Saita zowa mutanenta dashi, tana ɗauke dashi, sukace Ya Maryamu haƙiƙa kin aikata abu gundumeme, (da kika zoda ɗa ba tareda uba ba.)
27. Yake 'yar uwar Haruna, mutumne managarci ba Annabi Haruna ɗan uwan Annabi Musa ba,) babanki bai kasance mutumin banza ba, (mazinaci,) mahaifiyarki bata kasance karuwa ba, (to, ta ina kika sami wannan ɗa.)
28. Saitayi nuni (donsu) izuwa gareshi, (yi musu magana,) sukace, yaya zamuyi zance da wanda ya kasance (ƙanƙanen yaro) a cikin gunya.
29. Yace, " Haƙiƙa ni bawan Allah ne, ya bani Linjila, yasanya ni Annabi.
30. "Yasanya ni mai albarka inda duk na kasance (mai amfanin jama'a da abinda aka rubuta a gareshi,) yayi mini wasiyya da salla da zakka muddin ina rayayye.
31. "Yasanya ni mai biyayya ga mahaifiyata, bai sanya ni jabberi shaƙiyi ba.
32. "gaisuwa daga Allah ta tabbata gareni, ranar da aka haife ni da ranar mutuwatada ranar daza a tashe ni ina rayayye"

(KIRARIN ALLAH GA ANNABI ISA ALAHISSALAM DA TABBATAR DA BAUTARSA GA UBANGIJI MADAUKAKIN SARKI DA BAN TSORO DA RANAR LAHIRA GA WANDA YA SABESHI)

33. Wancananka shine Isa ɗan Maryamu alaihimasalamu,) Maganar gaskiya, wanda suke kokwanto cikinsa (sukace ɗan Allah ne don ƙarya.)
34. Bazai yiwu ga Allah ya riƙi wani ɗa ba, Allah ya kiyashe shi daga riƙon ɗa, idan yanufi farar da abu, sai kawai yace dashiya samu, saiya samu, to, (yana daga wannan halittar Annabi Isa bada uba ba.)
35. Haƙiƙa Allah shine Ubangijina, shine Ubangijinku, to, ku bauta masa tareda kaɗaitawa, wannan abin ambato, shine hanya madaidaici mai kaiwa izuwa aljanna.
36. To, sai kungiyoyin sukayi saɓani a tsakaninsu, (a cikin lamarin Annabi Isa Alaihissalam, waɗansu sukace ɗan Allah ne ko Allah ne, tareda Allah, ko na ukun uku ne,) Tsananin azaba ga waɗanda suka kafirta (da abinda aka ambata ɗin nan ya tabbata) daga halartar rana maigirma, (Itace ranar alƙiyama.)
37. Mana kin abinda yaji dasu! Mana kin abinda yaganar dasu, ranar da zasuzo mana a lahira, sai dai azzalumai a yau, (a duniya) suna cikin ɓata mabayyani, (sun kurunta ga buran jin gaskiya, sun makanta ga buran ganinta.)

وَأَنذِرْهُمْ يَوْمَ ٱلْحَسْرَةِ إِذْ قُضِيَ ٱلْأَمْرُ وَهُمْ فِي غَفْلَةٍ وَهُمْ
لَا يُؤْمِنُونَ ﴿38﴾ إِنَّا نَحْنُ نَرِثُ ٱلْأَرْضَ وَمَنْ عَلَيْهَا وَإِلَيْنَا يُرْجَعُونَ ﴿39﴾
ثمن * وَاذْكُرْ فِي ٱلْكِتَابِ إِبْرَاهِيمَ إِنَّهُ كَانَ صِدِّيقًا نَّبِيًّا ﴿40﴾
إِذْ قَالَ لِأَبِيهِ يَا أَبَتِ لِمَ تَعْبُدُ مَا لَا يَسْمَعُ وَلَا يُبْصِرُ وَلَا يُغْنِي عَنكَ
شَيْئًا ﴿41﴾ يَا أَبَتِ إِنِّي قَدْ جَاءَنِي مِنَ ٱلْعِلْمِ مَا لَمْ يَأْتِكَ فَاتَّبِعْنِي
أَهْدِكَ صِرَاطًا سَوِيًّا ﴿42﴾ يَا أَبَتِ لَا تَعْبُدِ ٱلشَّيْطَانَ إِنَّ ٱلشَّيْطَانَ
كَانَ لِلرَّحْمَٰنِ عَصِيًّا ﴿43﴾ يَا أَبَتِ إِنِّي أَخَافُ أَن يَمَسَّكَ عَذَابٌ
مِّنَ ٱلرَّحْمَٰنِ فَتَكُونَ لِلشَّيْطَانِ وَلِيًّا ﴿44﴾ قَالَ أَرَاغِبٌ أَنتَ
عَنْ ءَالِهَتِي يَا إِبْرَاهِيمُ لَئِن لَّمْ تَنتَهِ لَأَرْجُمَنَّكَ وَاهْجُرْنِي مَلِيًّا ﴿45﴾
قَالَ سَلَامٌ عَلَيْكَ سَأَسْتَغْفِرُ لَكَ رَبِّي إِنَّهُ كَانَ بِي حَفِيًّا ﴿46﴾
وَأَعْتَزِلُكُمْ وَمَا تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَأَدْعُو رَبِّي عَسَىٰ أَلَّا أَكُونَ
بِدُعَاءِ رَبِّي شَقِيًّا ﴿47﴾ فَلَمَّا اعْتَزَلَهُمْ وَمَا يَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ
وَهَبْنَا لَهُ إِسْحَاقَ وَيَعْقُوبَ وَكُلًّا جَعَلْنَا نَبِيًّا ﴿48﴾
وَوَهَبْنَا لَهُم مِّن رَّحْمَتِنَا وَجَعَلْنَا لَهُمْ لِسَانَ صِدْقٍ عَلِيًّا ﴿49﴾
وَاذْكُرْ فِي ٱلْكِتَابِ مُوسَىٰ إِنَّهُ كَانَ مُخْلَصًا وَكَانَ رَسُولًا نَّبِيًّا ﴿50﴾

38. Yi musu barazana (Ya Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama) da ranar nadama, (wato alƙiyama, a kan barin kyakkyawan aiki a duniya,) don an hukunta al'amari (garesu da azaba,) alhali su (a duniya) suna cikin rabkana (ga buransa,) su bazasu bada gaskiya (dashi) ba.
39. Haƙiƙa mu, mune muke gadon ƙasa da wanda yake kanta, izuwa garemu kaɗai suke komawa (saboda sakamako.)

(ƘISSAR ANNABI IBRAHIM ALAIHISSALAM,TA ƘUNSHI TAUSASAWA A CIKIN KIRA IZUWA ALLAH,DA TAUSAYIN MAHAIFI TA WAJEN SHIRYAR DASHI IZUWA ADDININ ALLAH DON GUDUN MUMMUNAN ƘARSHE)

40. Ambata musu labarin Annabi Ibrahim (Alaihissalam a cikin Alƙur'ani.)
41. Haƙiƙa shi, ya kasance mai yawan ban gaskiya, Annabi.
42. Zamanin daya faɗa ga baffansa [1] (Azaru) "Ya babana donme kake bautawa abinda bayaji baya gani baya wadatar da komai ga buranka, (na cuta ko amfani.)
43. "Ya babana, haƙiƙa wani abu na ilimi yazo mini wanda bai zo maka ba, to, bini in shiryeka tafarki madaidaici.
44. "Ya babana kadaka bautawa shaiɗan (wato kadaka bautawa gumaka,) haƙiƙa shaiɗan ya kasance mai yawan saɓone ga Ubangiji mai jinƙai.
45. "Ya babana, haƙiƙa ni ina jin tsoron azaba mai girma daga Ubangiji ta shafe ka (in baka tuba ba,) ka zama mataimaki ga shaiɗan (abokin zamansa a cikin wuta)".
46. Azaru yace, Shin! Kai ƙyama kakeyi ga buran iyayen gijina ya kai Ibrahim (kake laifanta ta?) Wallahi idan baka hanu ga buran kulawa da ita ba, zan jejjefe ka (da duwarwatsu, tareda asharce-asharce, hir dani!) kayi nesa dani zamani mai tsawo."
47. Annabi Ibrahim Alaihissalam yace, "Ranka ya daɗe, da sannu zan nema maka gafarar Ubangijina, haƙiƙa shiya tabbata mai yawan haba-habadani (zai amsa min addu'a. Yako roƙa masa gafarar, amma kafin yasanshi bazai bada gaskiya ba)
48. "Zan janye mukuda abinda kuke bautawa ba Allah ba, in bautawa Ubangijina, ina ƙauna bazan kasance taɓaɓɓe a wajen bautawa Ubangijina ba."
49. Yayin daya janye musu da abinda suke bautawa ba Allah ba, sai muka bashi "ya'ya guda biyu (dazai ɗebe kewa dasu, Ishakuda ya'aƙubu Alaihimassalamu,) kowane daga garesu mun sanyashi Annabi.
50. Mun basu daga rahamarmu dukiya da "ya"ya, mun sanya harshen gaskiya maɗaukaki a garesu. (Kyakkyawan yabo a cikin dukkan addinai.)

1) An ambaci ubansa bisa al'adar manya dasuke ambaton baffayo - uba. Amma mahaifi sunansa tarahu magana biyuce kowace tana da asali gurin masu tafsiri, (duba sawii).

وَنَٰدَيْنَٰهُ مِن جَانِبِ اِ۬لطُّورِ اِ۬لْأَيْمَنِ وَقَرَّبْنَٰهُ نَجِيّاً ﴿51﴾ وَوَهَبْنَا لَهُۥ مِن
رَّحْمَتِنَا أَخَاهُ هَٰرُونَ نَبِيٓـٔاً ﴿52﴾ وَاذْكُرْ فِي اِ۬لْكِتَٰبِ إِسْمَٰعِيلَ إِنَّهُۥ
كَانَ صَادِقَ اَ۬لْوَعْدِ وَكَانَ رَسُولاً نَّبِيٓـٔاً ﴿53﴾ وَكَانَ يَأْمُرُ أَهْلَهُۥ بِالصَّلَوٰةِ
وَالزَّكَوٰةِ وَكَانَ عِندَ رَبِّهِۦ مَرْضِيّاً ﴿54﴾ وَاذْكُرْ فِي اِ۬لْكِتَٰبِ
إِدْرِيسَ إِنَّهُۥ كَانَ صِدِّيقاً نَّبِيٓـٔاً ﴿55﴾ وَرَفَعْنَٰهُ مَكَاناً عَلِيّاً ﴿56﴾
أُوْلَٰٓئِكَ اَ۬لَّذِينَ أَنْعَمَ اَ۬للَّهُ عَلَيْهِم مِّنَ اَ۬لنَّبِيٓـِٔينَ مِن ذُرِّيَّةِ ءَادَمَ
وَمِمَّنْ حَمَلْنَا مَعَ نُوحٍ وَمِن ذُرِّيَّةِ إِبْرَٰهِيمَ وَإِسْرَٰٓءِيلَ وَمِمَّنْ هَدَيْنَا
وَاجْتَبَيْنَا إِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمُۥ ءَايَٰتُ اُ۬لرَّحْمَٰنِ خَرُّواْ سُجَّداً وَبُكِيّاً ﴿57﴾ *
* فَخَلَفَ مِنۢ بَعْدِهِمْ خَلْفٌ أَضَاعُواْ اُ۬لصَّلَوٰةَ وَاتَّبَعُواْ اُ۬لشَّهَوَٰتِ
فَسَوْفَ يَلْقَوْنَ غَيّاً ﴿58﴾ إِلَّا مَن تَابَ وَءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحاً فَأُوْلَٰٓئِكَ
يَدْخُلُونَ اَ۬لْجَنَّةَ وَلَا يُظْلَمُونَ شَيْـٔاً ﴿59﴾ جَنَّٰتِ عَدْنٍ اِ۬لَّتِي وَعَدَ اَ۬لرَّحْمَٰنُ عِبَادَهُۥ
بِالْغَيْبِ إِنَّهُۥ كَانَ وَعْدُهُۥ مَأْتِيّاً ﴿60﴾ لَّا يَسْمَعُونَ فِيهَا لَغْواً إِلَّا سَلَٰماً
وَلَهُمْ رِزْقُهُمْ فِيهَا بُكْرَةً وَعَشِيّاً ﴿61﴾ تِلْكَ اَ۬لْجَنَّةُ اُ۬لَّتِي نُورِثُ مِنْ
عِبَادِنَا مَن كَانَ تَقِيّاً ﴿62﴾ وَمَا نَتَنَزَّلُ إِلَّا بِأَمْرِ رَبِّكَ لَهُۥ مَا بَيْنَ
أَيْدِينَا وَمَا خَلْفَنَا وَمَا بَيْنَ ذَٰلِكَ وَمَا كَانَ رَبُّكَ نَسِيّاً ﴿63﴾

سجدة
ربع

AMBATON SASHIN ANNABAWA ALAIHIMUSSALAM, TA ƘUNSHI KIRARI GARESU DA KYAWAWAN HALAYE WANDA UBANGIJI YA BASU DONSU ZAMA MISALI A GAREMU MU KWAIKWAYESU A CIKINTA)

51. Ambaci Annabi Musa (Alaihissalam) a cikin alƙur'ani, haƙiƙa shiya kasance mai tsarkake aikinsa don Allah, ya kasance kuma jakadan Allah, Annabinsa.

52. Mun kirawo shi (inji Ubangiji, mukace Ya Musa, haƙiƙa ni, nine Allah,) daga nahiyar Duru [1] dutse mafi albarka, Muka kusanta shi abin ganawa dashi, (shine Ubangiji yaji dashi zancensa.)

53. Mukaba ɗan'uwansa Haruna Annabci tare dashi don jinƙanmu. (Wato mun amsawa Annabi Musa roƙonsa cewa a aiko ɗan uwansa tare dashi, gashi kuwa wa yake ga Annabi Musa tsiran Allah ya tabbata garesu).

54. Ka ambaci Annabi Isma'ila (Alaihissalam) a cikin Alƙur'ani, haƙiƙa shiya kasance magasgacin alƙawari, (bai taɓa alƙawarin abu ba face ya cika dashi, ya taɓa sauraron wada yayi masa alƙawari kwana uku ko shekara tum, har yakoma izuwa gareshiya sameshi a wannan gun.) Ya kasance jakada (Annabi izuwa Jurhum, da shari'ar Annabi Ibrahima alaihissalamu).

55. Ya kasance yana umarnin iyalinsa da salla da zakka, ya kasance yarjajje nan ga ubangijinsa.

56. ka ambaci Annabi Idrisa (Alai-hissalam) a cikin Alƙur'ani,(kakan uban Annabi Nuhu alaihis-salam domin Annabi Nuhu ɗan Lamkune ɗan Mattu - Shalihu ɗan Idrisu,) haƙiƙa ya kasance sadauki, Annabi.

57. Mun ɗaukaka shi mazauni maɗaukaki, (Yana cikin sama ta huɗu ko cikin aljanna bayan an ɗanɗana masa mutuwa an raya shi ba a fishshe shi daga cikinta ba.)

58. Waɗancananka ne waɗanda Allah yayi ni'ima a garesu na daga Annabawa na daga zuriyar Annabi Adamu (dan Idrisu,) kuma daga waɗanda muka ɗauka tareda Annabi Nuhu (a cikin jirgi, wato Annabi Ibrahimu da (ɗansa Samu,) daga zuriyar Annabi Ibrahima (ai Isma'ila da Ishaƙa da ya'aƙuba) daga zuriyar Isra'ila (Annabi Ya'aƙuba, ai Annabi Musa da Haruna da Zakariya'u da yahaya da isa tsiran Allah ya tabbata a garesu) daga waɗanda muka shiryesu muka zaɓesu. Idan ana karantawar ayoyin Ubangiji a garesu, sukan faɗi suna masu sajada masu kuka.

Sajada

(FIRGITARWA GA TOZARTA SALLA DA KWADAITARWA A KAN TUBADA BIYAYYA GA UBANGIJI)

59. Sai mutanen banza suka maye bayansu suka tozarta salla, (Yahudu da Nasara da makamantansu) sukabi sha'awace-sha'awace na saɓanni, da sannu zasu faɗa a cikin gwalalon jahannama.

60. Sai dai wanda ya tubaya bada gaskiya, yayi aiki nagari, to, waɗancananka zasu shiga aljanna, baza a tauye musu komai (na daga ladansu) ba.

61. Aljannatan dauwama waɗanda Ubangiji mai yawan jinƙai yayi wa bayinsa alƙawari suna fake ga buranta, (wato basu ganta ba,) alƙawarinsa kuwa ya kasance abin haɗuwa dashi.

62. Baza suji maganar banza a cikinta, ba sai dai gaisuwa (daga Mala'iku a garesu, ko daga ba'alinsu zuwa ba'ali,) arzikinsu na garesu a cikinta safiya dayammaci, (wato bisa gwargwadonsu a duniya don ita aljanna badare ba rana a cikinta, ita haskece har abada.)

63. Wancananka aljanna Itace wacce muke gadawa ɗukkan mai tsoron Allah daga bayinmu.

1) Dutse ne tsakanin Madayana da Misra, an anbace shi mafi albarka, don zamanin da Allah yayi tajjalli a gareshiya kasu kashi shida, kashi uku a Makka kashi uku a Madina, (duba wafa - Ul - wafa na shehu samhudi). - Sanajiy -

رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَا فَٱعۡبُدۡهُ وَٱصۡطَبِرۡ
لِعِبَٰدَتِهِۦۚ هَلۡ تَعۡلَمُ لَهُۥ سَمِيّٗا ﴿٦٥﴾ وَيَقُولُ ٱلۡإِنسَٰنُ أَءِذَا مَا مِتُّ
لَسَوۡفَ أُخۡرَجُ حَيًّا ﴿٦٦﴾ أَوَلَا يَذۡكُرُ ٱلۡإِنسَٰنُ أَنَّا خَلَقۡنَٰهُ
مِن قَبۡلُ وَلَمۡ يَكُ شَيۡـٔٗا ﴿٦٧﴾ فَوَرَبِّكَ لَنَحۡشُرَنَّهُمۡ وَٱلشَّيَٰطِينَ
ثُمَّ لَنُحۡضِرَنَّهُمۡ حَوۡلَ جَهَنَّمَ جِثِيّٗا ﴿٦٨﴾ ثُمَّ لَنَنزِعَنَّ مِن كُلِّ
شِيعَةٍ أَيُّهُمۡ أَشَدُّ عَلَى ٱلرَّحۡمَٰنِ عِتِيّٗا ﴿٦٩﴾ ثُمَّ لَنَحۡنُ أَعۡلَمُ
بِٱلَّذِينَ هُمۡ أَوۡلَىٰ بِهَا صِلِيّٗا ﴿٧٠﴾ وَإِن مِّنكُمۡ إِلَّا وَارِدُهَاۚ كَانَ
عَلَىٰ رَبِّكَ حَتۡمٗا مَّقۡضِيّٗا ﴿٧١﴾ ثُمَّ نُنَجِّي ٱلَّذِينَ ٱتَّقَواْ وَّنَذَرُ ٱلظَّٰلِمِينَ
فِيهَا جِثِيّٗا ﴿٧٢﴾ وَإِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٖ قَالَ ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ لِلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَيُّ ٱلۡفَرِيقَيۡنِ خَيۡرٞ مَّقَامٗا وَأَحۡسَنُ نَدِيّٗا ﴿٧٣﴾
وَكَمۡ أَهۡلَكۡنَا قَبۡلَهُم مِّن قَرۡنٍ هُمۡ أَحۡسَنُ أَثَٰثٗا وَرِءۡيٗا ﴿٧٤﴾
قُلۡ مَن كَانَ فِي ٱلضَّلَٰلَةِ فَلۡيَمۡدُدۡ لَهُ ٱلرَّحۡمَٰنُ مَدًّاۚ ﴿٧٥﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا رَأَوۡاْ
مَا يُوعَدُونَ إِمَّا ٱلۡعَذَابَ وَإِمَّا ٱلسَّاعَةَ فَسَيَعۡلَمُونَ مَنۡ هُوَ شَرّٞ
مَّكَانٗا وَأَضۡعَفُ جُندٗا ﴿٧٦﴾ وَيَزِيدُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ٱهۡتَدَوۡاْ هُدٗىۗ
وَٱلۡبَٰقِيَٰتُ ٱلصَّٰلِحَٰتُ خَيۡرٌ عِندَ رَبِّكَ ثَوَابٗا وَخَيۡرٞ مَّرَدًّا ﴿٧٧﴾

(JINKIRIN WAHAYI GA ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

Yayin da wahayi yayi jinkiri kwanuka, Annabi Sallallahu alaihi wasallama yace da jibrilu Alaihissalam, me ya hanaka ka ziyarce mune fiye dayadda kake ziyartarmu, sai Ubangiji yace:-"

64. Barna sauka saida umarnin Ubangijinka, abinda yake gabanmu (na al'amarin Lahira) na Allah ne, da abinda yake bayanmu (na al'amarin duniya) da abinda ke tsakanin wancananka, (har izuwa tashin alƙiyama, Allah kaɗai yake da wannan sani,) Ubangijinka bai kasance mai barinka ba saboda jinkirin wahayin nan.)
65. Shine Ubangijin sammai da ƙassai, da abinda ke tsakaninsu, ci gabada bautarsa ka daure a kanta, Shin kasan takwara gareshi? (A'a!)

MASU MUSUN TASHIN ALƘIYAMA DA SAKAMAKONSU)

66. Mutum mai musun tashin alƙiyama yana faɗa (Ubaiyu ɗan Halafu, ko Walidu dan Mugira) yanzu idan na mutu da sannu za a fitar dani daga ƙabari rarayye! Tamfar da Muhammadu (Sallallahu alaihi wasallama yake faɗa, sai Ubangiji yace:-)
67. "Yanzu wannan mutum baya tuna cewa haƙiƙa mu mun halicce shi tun gaba, alhali ba yana wani abu ba, (ya kafa dalili da fararsa a kan maidashi.)
68. To, na rantse da Ubangijinka, lallai zamu tara mamusa tashin alƙiyaman nan tareda shaidanunsu, sannan zamu halartar dasu gefen jahannama (ɗaga wajenta) Suna durƙushe (kan guyayinsu,)
69. Sannan zamu zare wanda yafi tsananin taurinkai ga Ubangiji daga kowace ƙungiya.
70. Sannan lallai mune masana da waɗanda suke mafi daidai a babbakawa da wuta.
71. Ba ɗaya daga cikinku face zai gangara a cikin jahannama, wannan ya kasance lallai tabbatacce daga Ubangijinka.
72. Sannan mu tserar da waɗanda sukaji tsoron Allah (basuyi shirka ba basuyi kafirci ba) mubar mushirikai a cikinta suna durƙushe (a kan guyayinsu.)

(GAJEREN HANZARI)

73. Idan ana karantawar ayoyinmu (na ƙur'ani) a garesu (mumunai da kafirai) halin kasancewarsu mabayyana, sai kafirai su faɗa ga waɗanda suka bada gaskiya, "Waɗanne ne daga jama'an nan guda biyu sukafi kyakkyawar mazauni, (mu koku,) sukafi kyan dandali."
74. (Ubangiji yace:) "Da yawa muka halakar da ƙarni gabansu, (wato al'umma daga al'umomi da suka wuce,) waɗandasu sukafi su kyan tarkace da magana (tamfar da muka halakar dasu saboda kafircinsu zamu halakar da waɗannan ma.)
75. Cene, "Wanda ya kasance a cikin ɓata, to, Ubangiji zaiyi masa talala ne talala.
76. "Har idan suka ga abinda ake musu alwashi imma azaba (kisa da ribacewa,) wa imma tashin alƙiyama, to, da sannu zasu san wanene yafi sharrin mazauni, yafi raunin runduna, (su ko muminai.)

ثمن

* أَفَرَأَيْتَ الَّذِي كَفَرَ بِـَٔايَٰتِنَا وَقَالَ لَأُوتَيَنَّ مَالًا وَوَلَدًا ﴿77﴾ أَطَّلَعَ
الْغَيْبَ أَمِ اتَّخَذَ عِندَ الرَّحْمَٰنِ عَهْدًا ﴿78﴾ كَلَّا سَنَكْتُبُ مَا يَقُولُ
وَنَمُدُّ لَهُ مِنَ الْعَذَابِ مَدًّا ﴿79﴾ وَنَرِثُهُ مَا يَقُولُ وَيَأْتِينَا فَرْدًا ﴿80﴾
وَاتَّخَذُوا مِن دُونِ اللَّهِ ءَالِهَةً لِيَكُونُوا لَهُمْ عِزًّا ﴿81﴾
كَلَّا سَيَكْفُرُونَ بِعِبَادَتِهِمْ وَيَكُونُونَ عَلَيْهِمْ
ضِدًّا ﴿82﴾ أَلَمْ تَرَ أَنَّا أَرْسَلْنَا الشَّيَٰطِينَ عَلَى الْكَٰفِرِينَ
تَؤُزُّهُمْ أَزًّا ﴿83﴾ فَلَا تَعْجَلْ عَلَيْهِمْ إِنَّمَا نَعُدُّ لَهُمْ عَدًّا ﴿84﴾
يَوْمَ نَحْشُرُ الْمُتَّقِينَ إِلَى الرَّحْمَٰنِ وَفْدًا ﴿85﴾ وَنَسُوقُ الْمُجْرِمِينَ
إِلَىٰ جَهَنَّمَ وِرْدًا ﴿86﴾ لَا يَمْلِكُونَ الشَّفَاعَةَ إِلَّا مَنِ
اتَّخَذَ عِندَ الرَّحْمَٰنِ عَهْدًا ﴿87﴾ وَقَالُوا اتَّخَذَ الرَّحْمَٰنُ
وَلَدًا ﴿88﴾ لَقَدْ جِئْتُمْ شَيْئًا إِدًّا ﴿89﴾ يَكَادُ السَّمَٰوَٰتُ
يَتَفَطَّرْنَ مِنْهُ وَتَنشَقُّ الْأَرْضُ وَتَخِرُّ الْجِبَالُ هَدًّا ﴿90﴾
أَن دَعَوْا لِلرَّحْمَٰنِ وَلَدًا ﴿91﴾ وَمَا يَنبَغِي لِلرَّحْمَٰنِ أَن يَتَّخِذَ وَلَدًا ﴿92﴾ إِن كُلُّ مَن
فِي السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ إِلَّا ءَاتِي الرَّحْمَٰنِ عَبْدًا ﴿93﴾ لَقَدْ أَحْصَىٰهُمْ
وَعَدَّهُمْ عَدًّا ﴿94﴾ وَكُلُّهُمْ ءَاتِيهِ يَوْمَ الْقِيَٰمَةِ فَرْدًا ﴿95﴾

77. Allah yana ƙarawa waɗanda suka shiriya shiriya ayyuka nagargaru masu wanzuwa ga masu su, sune sukafi kyakkyawan sakamako nan ga Ubangijinka. Sune sukafi kyakkyawar makoma.
78. Shin bamu labarin wanda ya kafirtada ayoyinmu (Asi dan Wa'ilu) yace da Habbabu (ɗan Arattu wanda yace dashi za a tasheka bayan ka mutu ka biya ni kuɗina, lallai za a bani dukiya da "ya"yaye in an tashe mu, na biya ka a can. Ubangiji yace:
79. Ya tsinkayi gaibu ne, (cewa za a bashi abinda yace,) ko kuwa ya riƙi alƙawari ne daga Allah.
80. Haggyala! Da sannu za a bayyana masa rubutaccen abinda ya faɗa, zamu ƙara masa ƙari na azaba.
81. Zamu gajeshi, izgilin nasa (na dukiya da ɗa,) zaizo mana santaran ba dukiyaba ɗa.

(MUSHIRIKAI)

82. Sun riƙi iyayen giji ba Allah ba gumaka dasuke bauta musu, donsu zama izza garesu (su cecesu kada ayi musu azaba.)
83. Haggyala! Da sannu zasu kafirce da bautarsu, zasu kasance kishiya a kansu.
84. Shin baka gani cewa haƙiƙa mun sallada shaiɗan a kan kafirai suna cunasu izuwa . saɓon Allah cunawa.
85. To, kada kayi garaje kansu da neman azaba, mudai muna ƙirga musu kwanaki ne da darairai da nunfarfashi ƙirgawa izuwa lokacin yi musu azaba.
86. Ka ambaci ranar da muke tara masu tsoron Allah izuwa Ubangiji mai jinƙai, suna baƙin girma.
87. Muke kora kafirai izuwa jahannama suna masu ƙishirwa.
88. Basu mallaki ceto ba sai wanda ya riƙi alƙawari daga ubangiji (shaidawa ba wani abin bautawa da gaskiya sai Allah, Annabi Muhammadu kuma manzon Allah ne ba tsimi badabara saida nufin Allah)

(ƘIRƘIRAN RIƘON DA) "YAHUDU DA NASARA DA MASU KAMA DASU"

89. Sukace, "Ubangiji ya riƙi ɗa.
90. (Ubangiji yace dasu) "Lallai haƙiƙa kun zoda abu gingimeme".
91. Sammai suna kusanta su kyarkece saboda shi, ƙassaisu rugurguje duwarwatsu su rushe, rushewa.
92. Don sunyi da'awar ɗa ga Ubangiji mai rahama.
93. Ubangiji yace- Bai kamata ga ubangiji ya riƙi ɗa ba.
94. Duk wanda yake cikin sammai da ƙassai bai kasance ba, face mai zowa Ubangiji ne yana bawa, (Uzairu da Isa suna cikinsu.)
95. Haƙiƙa Ubangiji ya kewaye da saninsu, ya ƙirge su ƙirga.

إِنَّ الَّذِينَ ءَامَنُوا وَعَمِلُوا الصَّٰلِحَٰتِ سَيَجْعَلُ لَهُمُ الرَّحْمَٰنُ وُدًّا ﴿96﴾
فَإِنَّمَا يَسَّرْنَٰهُ بِلِسَانِكَ لِتُبَشِّرَ بِهِ الْمُتَّقِينَ وَتُنذِرَ بِهِ قَوْمًا لُّدًّا ﴿97﴾
وَكَمْ أَهْلَكْنَا قَبْلَهُم مِّن قَرْنٍ هَلْ تُحِسُّ مِنْهُم مِّنْ أَحَدٍ أَوْ تَسْمَعُ لَهُمْ رِكْزًا ﴿98﴾

سُورَةُ طه مَكِّيَّةٌ 20

وَهِيَ مِائَةٌ وَأَرْبَعٌ وَثَلَاثُونَ ءَايَةً 134

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

* طه ﴿1﴾ مَا أَنزَلْنَا عَلَيْكَ الْقُرْءَانَ لِتَشْقَىٰ ﴿2﴾ إِلَّا تَذْكِرَةً لِّمَن
يَخْشَىٰ ﴿3﴾ تَنزِيلًا مِّمَّنْ خَلَقَ الْأَرْضَ وَالسَّمَٰوَٰتِ الْعُلَى ﴿4﴾
الرَّحْمَٰنُ عَلَى الْعَرْشِ اسْتَوَىٰ ﴿5﴾ لَهُ مَا فِي السَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ
وَمَا بَيْنَهُمَا وَمَا تَحْتَ الثَّرَىٰ ﴿6﴾ وَإِن تَجْهَرْ بِالْقَوْلِ
فَإِنَّهُ يَعْلَمُ السِّرَّ وَأَخْفَى ﴿7﴾ اللَّهُ لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ
لَهُ الْأَسْمَاءُ الْحُسْنَىٰ ﴿8﴾ وَهَلْ أَتَىٰكَ حَدِيثُ مُوسَىٰ ﴿9﴾ إِذْ رَءَا نَارًا
فَقَالَ لِأَهْلِهِ امْكُثُوا إِنِّي ءَانَسْتُ نَارًا لَّعَلِّي ءَاتِيكُم مِّنْهَا بِقَبَسٍ
أَوْ أَجِدُ عَلَى النَّارِ هُدًى ﴿10﴾ فَلَمَّا أَتَىٰهَا نُودِيَ يَٰمُوسَىٰ ﴿11﴾ إِنِّي
أَنَا رَبُّكَ فَاخْلَعْ نَعْلَيْكَ إِنَّكَ بِالْوَادِ الْمُقَدَّسِ طُوًى ﴿12﴾

حزب

96. Dukkansu zasuzo masa ranar alƙiyama kwal ba dukiyaba mataimaki.
97. Haƙiƙa waɗanda suka bada gaskiya, sukayi aiki nagargaru da sannu Ubangiji zai sanya musu soyayya a tsakaninsu da juna kuma (yaso su.)
98. To, mudai kawai mun sauwaƙe maka wannan alƙur'anine da harshenka, Balarabe, don kayi albishir dashi ga masu tsoron Allah, ka firgita mutane taƙadaru dashi.
99. Da yawa muka halakar nadaga ƙarni gabansu saboda ƙaryata manzanni, shin kana hasashen ɗaya daga garesu ko kanajin motsinsu (A'a! To, kamar yadda muka halakar da waɗancan zamu halakar da waɗannan.)

Suratu Dahe

A Makka Aka. Saukar Da Ita Ayoyinta Dari Da Talatin Da Huɗu. (134)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabaɗaya mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe

'Ita wannan sura tana iyakance cewa Sayyaduna Rasulullahi Sallallahu alaihi wasallama jakadan Allah ne bai mallaki komai sai isar da aike, yana tare dashi bai bar shi bakamar yadda al'ada ga sauran Annabawa, kamar Annabi Musa da waɗanda suka gasgata shi. Ta ƙunshi gar-gaɗi da ranar alƙiyama da bayanin ƙissar Annabi Adamu Alaihissalam don "ya"yansa su wa'azantu kadasu amince da sharrin shaiɗan."

(KULAWA DA SAYYADINA RASULULLAHI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA DA MATUƘAR BAN GIRMA DA TAUSA-SAWA A CIKIN ZANCE DASHI)

1. Ya wannan Annabi maigirma abin kira da wannan suna, bamu saukar da Alƙur'ani a gareka donka wahala ba, (ai donka wahala daga abinda ka aikata bayan saukar sa na daga tsawon tsaiwar da sallar dare, wato sauwaƙewa kanka.)
2. Sai dai mun saukar dashine don kayi gargaɗi dashi ga wanda yake tsoron Allah.
3. Don saukarwa daga wanda ya halicci ƙassai da sammai maɗaukaka.
4. Shine Ubangiji Arrahmanu, yayi daidai a kan Al'arshi, gadon sarauta,
5. Abinda yake sammai da abinda yake ƙassai nasa ne, da abinda yake tsakaninsu (nadaga ababen halitta) da abinda yake ƙarƙashin turɓaya mai danshi (abinda ake nufi da ƙassai bakwai, domin su suna ƙarƙashin Al'arshi.)
6. Idan ka bayyana da addu'a ko zikiri, (Allah mawadaci ne ga buran bayyanawarka dashi) to, haƙiƙa shi yasan asirin fake da mafi ɓuya daga gareshi (wato zancen zuci).
7. To, Allah ba abin bautawa da gaskiya sai shi, sunannaki kyawawa sun tabbata gareshi, (guda ɗari ɗaya babu.)

(ƘSSAR ANNABI MUSA ALAIHISSALAM TAREDA FIR'AUNA DA BANI ISRA'ILA)

8. Haƙiƙa labarin Annabi Musa yazo maka.
9. Yayin dayaga wuta, yace da mata tasa "Ku zauna a nan, (wancananka a cikin tafiyarsa ne daga Madayyana zuwa Misra,) haƙiƙani na hangi wuta, ƙila nazo mukuda dosana daga gareta, ko na samu shiryarwa a kan wuta, (alhali ya bacewa hanya saboda duhun dare, yace wata kila saboda bai yanke da cikar alƙawarin ba.)
10. A yayin dayazo mata, (wato itaciyar dundu ce,) sai aka kira shi, "Ya Musa.
11. " Haƙiƙa ni, nine Ubangijinka, tuɓe takalmanka, kai haƙiƙa kana zaza abin tsarkakewa (shine Duwa.)

وَأَنَا اخْتَرْتُكَ فَاسْتَمِعْ لِمَا يُوحَىٰ ﴿12﴾ إِنَّنِي أَنَا اللَّهُ لَا إِلَٰهَ إِلَّا
أَنَا فَاعْبُدْنِي وَأَقِمِ الصَّلَوٰةَ لِذِكْرِيٓ ﴿13﴾ إِنَّ السَّاعَةَ ءَاتِيَةٌ
أَكَادُ أُخْفِيهَا لِتُجْزَىٰ كُلُّ نَفْسِۭ بِمَا تَسْعَىٰ ﴿14﴾ فَلَا يَصُدَّنَّكَ
عَنْهَا مَن لَّا يُؤْمِنُ بِهَا وَاتَّبَعَ هَوَاهُ فَتَرْدَىٰ ﴿15﴾ وَمَا تِلْكَ
بِيَمِينِكَ يَٰمُوسَىٰ ﴿16﴾ قَالَ هِيَ عَصَايَ أَتَوَكَّؤُا عَلَيْهَا وَأَهُشُّ
بِهَا عَلَىٰ غَنَمِي وَلِيَ فِيهَا مَـَٔارِبُ أُخْرَىٰ ﴿17﴾ قَالَ أَلْقِهَا يَٰمُوسَىٰ ﴿18﴾
فَأَلْقَاهَا فَإِذَا هِيَ حَيَّةٌ تَسْعَىٰ ﴿19﴾ قَالَ خُذْهَا وَلَا تَخَفْ
سَنُعِيدُهَا سِيرَتَهَا الْأُولَىٰ ﴿20﴾ وَاضْمُمْ يَدَكَ إِلَىٰ جَنَاحِكَ
تَخْرُجْ بَيْضَآءَ مِنْ غَيْرِ سُوٓءٍ ءَايَةً أُخْرَىٰ ﴿21﴾ لِنُرِيَكَ مِنْ ءَايَٰتِنَا
الْكُبْرَى ﴿22﴾ اذْهَبْ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ إِنَّهُ طَغَىٰ ﴿23﴾ * قَالَ رَبِّ اشْرَحْ لِي
صَدْرِي ﴿24﴾ وَيَسِّرْ لِيٓ أَمْرِي ﴿25﴾ وَاحْلُلْ عُقْدَةً مِّن لِّسَانِي ﴿26﴾
يَفْقَهُوا قَوْلِي ﴿27﴾ وَاجْعَل لِّي وَزِيرًا مِّنْ أَهْلِي ﴿28﴾ هَٰرُونَ أَخِي ﴿29﴾
اشْدُدْ بِهِۦٓ أَزْرِي ﴿30﴾ وَأَشْرِكْهُ فِيٓ أَمْرِي ﴿31﴾ كَيْ نُسَبِّحَكَ كَثِيرًا ﴿32﴾
وَنَذْكُرَكَ كَثِيرًا ﴿33﴾ إِنَّكَ كُنتَ بِنَا بَصِيرًا ﴿34﴾ قَالَ قَدْ أُوتِيتَ
سُؤْلَكَ يَٰمُوسَىٰ ﴿35﴾ وَلَقَدْ مَنَنَّا عَلَيْكَ مَرَّةً أُخْرَىٰ ﴿36﴾

ثمن

12. "Ni na zaɓe ka daga mutanenka, saurari abinda ake aikowa daga gareni (izuwa gareka.)
13. " Haƙiƙa ni, Nine Allah, ba abin bautawa da gaskiya sai ni, to, bauta min, ka tsayar da salla donka ambace ni (a cikinta).
14. " Haƙiƙa Alƙiyama mai zuwa ce, ina kusa in ɓoyeta ga buran mutane kusancinta ya bayyana garesu (da alamominta,) don a saka wa kowace kai abindata aikata (na hairi ko sharri.)
15. "Kada wanda bai bada gaskiya da ita baya juyar dakai ga buranta, yabi son zuciya tasa (a cikin musunta) ka halaka."

AIKO ANNABI MUSA DA ABINDA YA NEMA DAGA UBANGIJINSA)

16. (Yace). "mece ce a hannun da-marka ya annabi Musa!
17. "Ita sandatace, nake dogaro kanta (yayin zabura da tafiya) nake kaɗo ganye da ita a kan tumakaina, ina da buƙatu da yawa a cikinta, (kamar ɗaukar guzuri da salka da korewar namun jeji".)
18. Yace, "Jefar da ita Ya Musa".
19. Sai yajefar da ita, kumfa sai ga ta tana micijiya tana tafe a kan cikinta.
20. Yace, " Riƙe ta kada kaji tsoronta, da sannu zamu mayar da ita halinta na farko (An nuna wa Annabi Musa don kada ya ji tsoro in ta kuma zama macijiya nan ga Fir'auna, saiya shigar da hannunsa cikin bakinta saita koma sanda, saita bayyana gareshi cewa; wajen shigar wannan shine wurin riƙe ta tsakanin gyaffanta.)
21. "Tara hannunka (na dama) izu-wa hammatarka (ta hagun ƙarkashin dantsenka izuwa hammatarka, fitar da ita,) ta fito fara fat ba tareda muni ba, (albaras) tana haske kamar hasken rana tana disashe idanu,) aya wata daban.
22. "Don mu nuna maka (idan ka aikata wannan) daga ayoyinmu aya mafi girma. (Idan yanufi komawarta saiya shigar da ita cikin hammatarsa yafitar da ita.)
"Jeka kana jakada izuwa Fir'auna da wanda yake tare dashi, haƙika shi yayi shisshigi (yayi da'awar Allantaka.")
24. Sai yace, "Ubangijina buɗe min ƙirjina (saboda ɗaukar saƙo.)
25. "Ka sauwake min al'amarin (don in iyar da ita.)
26. "Ka kwance gura-gura daga harshena data faru daga konewa tasa ga bakinsa yana ɗan ƙaramin yaro.)
27. "Donsu fahimci maganata (yayin ida aike).
28. "Ka sanya min waziri daga iyalina.
29. "Shine Haruna ɗan uwana."
30. "In ƙarfafa bayana dashi."
31. "tara shi a cikin al'amarina na aike."
32. "Don mu yi tasbihi gareka mai yawa.
33. "Mu ambaceka ambato mai yawa."
34. " Haƙiƙa kai ka kasance masani damu."

(ALDAFULLAHI WAƊANDA SUKA SAMI ANNABI MUSA ALAIHISISALAM.)

35. (Yace,) Haƙiƙa an baka muradinka Ya Annabi Musa (Alaihissalam, saboda kyauiawa a gareka.)
36. Haƙiƙa mun kyauta a gareka wata marra dabam.

إِذْ أَوْحَيْنَا إِلَىٰ أُمِّكَ مَا يُوحَىٰ ﴿37﴾ أَنِ اقْذِفِيهِ فِي التَّابُوتِ فَاقْذِفِيهِ
فِي الْيَمِّ فَلْيُلْقِهِ الْيَمُّ بِالسَّاحِلِ يَأْخُذْهُ عَدُوٌّ لِّي وَعَدُوٌّ لَّهُ
وَأَلْقَيْتُ عَلَيْكَ مَحَبَّةً مِّنِّي ﴿38﴾ وَلِتُصْنَعَ عَلَىٰ عَيْنِي ﴿39﴾ إِذْ تَمْشِي أُخْتُكَ
فَتَقُولُ هَلْ أَدُلُّكُمْ عَلَىٰ مَن يَكْفُلُهُ فَرَجَعْنَاكَ إِلَىٰ أُمِّكَ
كَيْ تَقَرَّ عَيْنُهَا وَلَا تَحْزَنَ وَقَتَلْتَ نَفْسًا فَنَجَّيْنَاكَ مِنَ الْغَمِّ وَفَتَنَّاكَ
فُتُونًا فَلَبِثْتَ سِنِينَ فِي أَهْلِ مَدْيَنَ ثُمَّ جِئْتَ عَلَىٰ قَدَرٍ يَا مُوسَىٰ ﴿40﴾
وَاصْطَنَعْتُكَ لِنَفْسِي اذْهَبْ أَنتَ وَأَخُوكَ بِآيَاتِي وَلَا تَنِيَا
فِي ذِكْرِي ﴿41﴾ اذْهَبَا إِلَىٰ فِرْعَوْنَ إِنَّهُ طَغَىٰ ﴿42﴾ فَقُولَا لَهُ قَوْلًا لَّيِّنًا
لَّعَلَّهُ يَتَذَكَّرُ أَوْ يَخْشَىٰ ﴿43﴾ قَالَا رَبَّنَا إِنَّنَا نَخَافُ أَن يَفْرُطَ
عَلَيْنَا أَوْ أَن يَطْغَىٰ ﴿44﴾ قَالَ لَا تَخَافَا إِنَّنِي مَعَكُمَا أَسْمَعُ
وَأَرَىٰ ﴿45﴾ فَأْتِيَاهُ فَقُولَا إِنَّا رَسُولَا رَبِّكَ فَأَرْسِلْ مَعَنَا بَنِي إِسْرَائِيلَ
وَلَا تُعَذِّبْهُمْ قَدْ جِئْنَاكَ بِآيَةٍ مِّن رَّبِّكَ وَالسَّلَامُ عَلَىٰ مَنِ اتَّبَعَ
الْهُدَىٰ ﴿46﴾ إِنَّا قَدْ أُوحِيَ إِلَيْنَا أَنَّ الْعَذَابَ عَلَىٰ مَن كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰ ﴿47﴾
قَالَ فَمَن رَّبُّكُمَا يَا مُوسَىٰ ﴿48﴾ قَالَ رَبُّنَا الَّذِي أَعْطَىٰ كُلَّ
شَيْءٍ خَلْقَهُ ثُمَّ هَدَىٰ ﴿49﴾ قَالَ فَمَا بَالُ الْقُرُونِ الْأُولَىٰ ﴿50﴾

37. Don mun aiko izuwa mahaifiy-arka a mafarki, (wato mun kimsa mata, yayin data haifeka ta ji tsoron Fir'auna ya kashe ka a cikin jimlar wađanda ake haifa,) muka kimsa mata abinda ake kimsawa a cikin sha'aninka.
38. Shine ki jefa shi a cikin akwatu, kuma ki jefa shi tareda akwatunnan a cikin kogin Nil, ta jefa shı (a geffan kogin,) magaucina magaucinsa ya đauke shi (shine Fir'auna,) na jefa soyayya daga gareni a gareka, (saboda haka Fir'auna yaso kada duk wanda yaganka.)
39. Kuma don a raine ka a bisa kulawata.
40. Don 'yar uwarka tana tafiya (Maryamu don nemo labarinka, alhali sun halarto da mataye masu shayarwa, kai baka yarda da nonon ko daya badaga cikinsu) tana cewa bana shiryar dakubisa wandazai rene shi ba? (Aka amsa mata, saita zoda mahaifiyarsa, ya karɓi nononta,) Muka mayar dakai izuwa mahaifiyarka don idaniyarta ta sanyaya, baza tayi baƙin ciki ba. A yayin nan ka kashe rai, (shine Bakibđe a Misra, kayi baƙin cikin kashe shi, daga jihar Fir'auna,) Muka tserar dakai daga baƙin cikin, muka jarrabe ka jarraba (da afkar dakai cikin wannan da kuma kubutar dakai daga gareshi) ka zauna shekara goma a cikin mutanen Madayana, (bayan zuwanka izuwa gareta daga Misra daga Annabi Sha'aibu Alaihissalam, da auren ka "yarsa, sannan) kazo bisa daidai wadaida (da aike a cikin sanina shine shekara arba'in daga shekarunka,) Ya Musa (alaikassalamu!)
41. Nayi tattalinka ga aike don kaina, sai ka tafi kai da dan uwanka (izuwa mutane) da ayoyina guda tara, kada kuyi sake a cikin ambatona.

(KIRAN ANNABI MUSA ALAIHISSALAM GA FIR'AUNA DA HUJJA-TAYYADASHI)

42. Ku tafi izuwa Fir'auna, haƙiƙa shi yayi shisshigi (da da'awar Allantaka,)
43. Ku gaya masa magana mai lau-shi (a cikin komowarsa ga buran wancananka, koya wa'azantu yaji tsoron Allah. (Dangane da ƙaunar da Annabi Musa da dan uwansa sukeyi, amma Ubangiji yasan bazai komo ba.)
44. Sukace, "Ya Ubangijinmu, mu muna jin tsoron yai dim a kanmu da azaba, "ko yai đagawa".
45. Yace, "Kada kuji tsoro, ni ina taredaku ,(da taimakona,) ina jin (abindazai fađa,) ina ganin (abinda zai aikata.)
46. "Ku je masa ku ce; Mu haƙiƙa jakadun Ubangijinka ne, ka sako Bani-Isra'ila tareda mu (izuwa Sham,) kada kayi musu azaba, (da aiwatarsu cikin aikace. aikace na wahala da kake yi, kamar hakan rami da gini da daukar kaya mai nauyi.) Haƙiƙa mun zo maka da hujja daga Ubangijinka (mai shiryarwa bisa gaskiyarmu da jakadanci.) Tsira ya tabbata ga wanda yabi shiriya (Allah bazai masa azaba ba.)
47. " Haƙiƙa mu, an aiko izuwa garemu cewa Lallai azaba tana kan wanda ya ƙaryatada abinda nazo dashi ya juya bayansa ga buransa. (Suka je masa, suka gaya masa duk abinda aka ambata đin nan.
48. Yace, "Wanene Ubangijinkune Ya Musa!"
49. Yace, "Ubangijinmu wanda ya baiwa kowane abu sura tasa (da kamanninsa) sannan ya shiryi (mai rai daga gareshi izuwa abincinsa da shansa da mazauninsa da wanin wannan.)
50. Fir'auna yace, "Menene halin al'ummatai ne farko, (kamar mutanen Annabi Nuhu, da Hudu da Luđu da Salihu alaihimussalamu a cikin bauta -warsu gagumaka".)

قَالَ عِلْمُهَا عِندَ رَبِّي فِي كِتَٰبٖ لَّا يَضِلُّ رَبِّي وَلَا يَنسَى ﴿51﴾
اَ۬لذِے جَعَلَ لَكُمُ اُ۬لْأَرْضَ مِهَٰداٗ وَسَلَكَ لَكُمْ فِيهَا سُبُلاٗ
وَأَنزَلَ مِنَ اَ۬لسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَخْرَجْنَا بِهِۦٓ أَزْوَٰجاٗ مِّن نَّبَاتٖ شَتَّيٰ ﴿52﴾
كُلُواْ وَارْعَوْاْ أَنْعَٰمَكُمُۥٓ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّأُوْلِے اِ۬لنُّهَيٰ ﴿53﴾
* مِنْهَا خَلَقْنَٰكُمْ وَفِيهَا نُعِيدُكُمْ وَمِنْهَا نُخْرِجُكُمْ تَارَةً اُخْرَيٰ ﴿54﴾ ربع
وَلَقَدْ أَرَيْنَٰهُ ءَايَٰتِنَا كُلَّهَا فَكَذَّبَ وَأَبَيٰ ﴿55﴾ قَالَ أَجِئْتَنَا
لِتُخْرِجَنَا مِنْ أَرْضِنَا بِسِحْرِكَ يَٰمُوسَيٰ ﴿56﴾ فَلَنَأْتِيَنَّكَ بِسِحْرٖ مِّثْلِهِۦ
فَاجْعَلْ بَيْنَنَا وَبَيْنَكَ مَوْعِداٗ لَّا نُخْلِفُهُۥ نَحْنُ وَلَا أَنتَ مَكَاناٗ
سِوىٗ ﴿57﴾ قَالَ مَوْعِدُكُمْ يَوْمُ اُ۬لزِّينَةِ وَأَن يُحْشَرَ اَ۬لنَّاسُ ضُحيٗ ﴿58﴾
فَتَوَلَّيٰ فِرْعَوْنُ فَجَمَعَ كَيْدَهُۥ ثُمَّ أَتَيٰ ﴿59﴾ قَالَ لَهُم مُّوسَيٰ وَيْلَكُمْ
لَا تَفْتَرُواْ عَلَى اَ۬للَّهِ كَذِباٗ فَيُسْحِتَكُم بِعَذَابٖ وَقَدْ خَابَ
مَنِ اِ۪فْتَرَيٰ ﴿60﴾ فَتَنَٰزَعُوٓاْ أَمْرَهُم بَيْنَهُمْ وَأَسَرُّواْ اُ۬لنَّجْوَيٰ ﴿61﴾
قَالُوٓاْ إِنَّ هَٰذَٰنِ لَسَٰحِرَٰنِ يُرِيدَانِ أَن يُخْرِجَٰكُم مِّنْ أَرْضِكُم
بِسِحْرِهِمَا وَيَذْهَبَا بِطَرِيقَتِكُمُ اُ۬لْمُثْلَيٰ ﴿62﴾ فَأَجْمِعُواْ كَيْدَكُمْ
ثُمَّ اُ۪يتُواْ صَفّاٗ وَقَدْ أَفْلَحَ اَ۬لْيَوْمَ مَنِ اِ۪سْتَعْلَيٰ ﴿63﴾

51. Annabi Musa yace, "Sanin halinsu yana gurin Ubangijina a cikin Lauhul-Mahfuzu, (za ayi musu sakamako da ita a ranar tashin alƙiyama,) Ubangijina baya fakuwa (ga buran wani abu) kuma baya mancewa.
52. "Shine wanda yasanya muku ƙasa shinfiɗa, ya shigar daku ,cikin hanyoyi ya saukar da ruwa daga sama, yasanya muku hanyoyi a cikinta, ya saukar da ruwa daga sama muka fitar da nau'o'in tsire- tsire dabandaban."
53. "Kuci daga gareta, ku shayar da dabbobinku, haƙiƙa a cikin wancananka akwai ayoyi ga ma'abuta hankula.

(DAN ADAM BAZAI ZAUNA A DU-NIYAR WATA KO TA TAURARO BA)

54. Daga cikin ƙasa muka halicce ku (saboda mun halicci ubanku Annabi Adamu daga gareta) a cikinta zamu mayar daku ,(a ƙabari bayan kun mutu,) daga cikinta zamu fitar daku ,(yayin tashin alƙiyama) wani yayi (tamfar dà muka fishshe ku yayin fara halittar ku.)

(ƘARSHEN MAGANAR FIR'AUNA)

55. Haƙiƙa mun nuna wa Fir'auna ayoyinmu (guda tara) dukkanta saiya ƙaryata ta yaki kadaita Ubangiji. yace tsafi ce.

(ANNABI MUSA ALAIHISSALAM TAREDA MATSAFA WAƊANDA FIR'AUNA YA TARA SU)

56. (Fir'auna) yace, Shin kazo mana ne donka fishshe mu daga ƙasarmune (Misra) ka zama kaine kaɗai zaka sarauce tada sihirinka Ya Musa?
57. "To, lallai zamu zo maka da tsafi irinsa (dazai bijirereniya dashi,) sanya alƙawari tsakaninmu dakai (saboda wannan, mu) bazamu sabashi bakai ma haka a guri madaidaici (wandazai zama daidai ga masu zuwa (gyaffan biyu).
58. Annabi Musa alaihissalam yace, alƙawarinku ranar ado (wato ranar idinsu) suna tat tara, kuma a tara mutane da walaha.")
59. Sai Fir'auna ya bada baya, sannan ya tattara kaidinsa (na tsafi) sannan yazo (dasu gurin alƙawarin nan)
60. Annabi musa (Alaihissalam) yace (musu alhali su saba'in da biyu ne (72) akwai sanda da igiya tareda kowane ɗaya daga cikinsu)" Kaiconku! Kadaku ,kuta ƙarya bisa Ubangiji, kadaku ,tara wani tare dashi a bauta, saboda haka ya rangade kuda azaba (daga gareshi) haƙiƙa wanda yakuta ƙaryaga Allah ya taɓe.
61. Sukayi jayayyar al'amarinsu a tsakaninsu (cikin Annabi Musa da dan uwansa,) suka ɓoye zance tsakaninsu, (na Annabi Musa da Haruna alaihimussalamu.)
62. Suka faɗa (ga kawunansu,) " Haƙiƙa waɗannan biyun nan lallai matsafa ne suna nufin fishshe ku daga ƙasarku, da tsafinsu, su tafi da sarautarku mafificiya.
63. "Ku kyautata kaidunku, sannan kuzo a dunƙule, haƙiƙa wanda yayi rinjaye a yau ya rabauta."

قَالُوا يَٰمُوسَىٰٓ إِمَّآ أَن تُلْقِيَ وَإِمَّآ أَن نَّكُونَ أَوَّلَ مَنْ أَلْقَىٰ ﴿64﴾
قَالَ بَلْ أَلْقُوا۟ فَإِذَا حِبَالُهُمْ وَعِصِيُّهُمْ يُخَيَّلُ إِلَيْهِ مِن سِحْرِهِمْ أَنَّهَا
تَسْعَىٰ ﴿65﴾ فَأَوْجَسَ فِى نَفْسِهِۦ خِيفَةً مُّوسَىٰ ﴿66﴾ قُلْنَا لَا تَخَفْ
إِنَّكَ أَنتَ ٱلْأَعْلَىٰ ﴿67﴾ وَأَلْقِ مَا فِى يَمِينِكَ تَلْقَفْ مَا صَنَعُوٓا۟ إِنَّمَا صَنَعُوا۟
كَيْدُ سَٰحِرٍ وَلَا يُفْلِحُ ٱلسَّاحِرُ حَيْثُ أَتَىٰ ﴿68﴾ فَأُلْقِىَ ٱلسَّحَرَةُ سُجَّدًا قَالُوٓا۟ ءَامَنَّا
بِرَبِّ هَٰرُونَ وَمُوسَىٰ ﴿69﴾ قَالَ ءَامَنتُمْ لَهُۥ قَبْلَ أَنْ ءَاذَنَ لَكُمْ إِنَّهُۥ لَكَبِيرُكُمُ
ٱلَّذِى عَلَّمَكُمُ ٱلسِّحْرَ فَلَأُقَطِّعَنَّ أَيْدِيَكُمْ وَأَرْجُلَكُم مِّنْ خِلَٰفٍ
وَلَأُصَلِّبَنَّكُمْ فِى جُذُوعِ ٱلنَّخْلِ وَلَتَعْلَمُنَّ أَيُّنَآ أَشَدُّ عَذَابًا وَأَبْقَىٰ ﴿70﴾
* قَالُوا۟ لَن نُّؤْثِرَكَ عَلَىٰ مَا جَآءَنَا مِنَ ٱلْبَيِّنَٰتِ وَٱلَّذِى فَطَرَنَا ثمن
فَٱقْضِ مَآ أَنتَ قَاضٍ إِنَّمَا تَقْضِى هَٰذِهِ ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَآ ﴿71﴾ إِنَّآ ءَامَنَّا بِرَبِّنَا
لِيَغْفِرَ لَنَا خَطَٰيَٰنَا وَمَآ أَكْرَهْتَنَا عَلَيْهِ مِنَ ٱلسِّحْرِ
وَٱللَّهُ خَيْرٌ وَأَبْقَىٰٓ ﴿72﴾ إِنَّهُۥ مَن يَأْتِ رَبَّهُۥ مُجْرِمًا فَإِنَّ لَهُۥ جَهَنَّمَ لَا يَمُوتُ
فِيهَا وَلَا يَحْيَىٰ ﴿73﴾ وَمَن يَأْتِهِۦ مُؤْمِنًا قَدْ عَمِلَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
فَأُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلدَّرَجَٰتُ ٱلْعُلَىٰ ﴿74﴾ جَنَّٰتُ عَدْنٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا
ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا وَذَٰلِكَ جَزَآءُ مَن تَزَكَّىٰ ﴿75﴾

64. Sukace, "Ya Musa (ka zaba) imma ka jefa (sandarka da farko) ko mu kasance farkon wandazai jefa (sandarsa.)"
65. Yace, "A'a, kujefa ku, (sai suka jefa,) sai ga igiyoyinsu da sandunansu ana surantawa gareshi don tsafinsu cewa su haƙiƙa macizai ne da take jan ciki.
66. Sai Annabi Musa (alaihissalam) ya darsa tsoro cikin ransa.
67. Mukace (dashi) "Kada kaji tsoro, haƙiƙa kai kaine mafi ɗaukaka (kansu da rinjaye.)"
68. Jefa abinda yake cikin damtsenka (wato sandata caccafe abinda suka aikata, abinda suka aikata din nan kaidin matsafi ne kawai, matsafi ko bazai rabauta baindadukyaje.
69. Matsafa suka faɗi suna masu sajada, Sukace, "Mun bada gaskiya da Ubangijin Annabi Haruna da Annabi Musa (alaihimussalamu).
70. Fir'auna yace, "To, bada gaskiya kukayi dashi tun gaban ban baku izini dashi ba. Haƙiƙa shine babban malaminku wanda yasanar daku ,tsafi, to, lallai zan yanyanke hannayenkuda kafafuwanku a kaikaice, (hannuwan dama da kafafuwan hagu,) Lallai zan tsire ku a kan ginshikan dabino. Lallai zaku sami wannenenmu yafi tsananin azaba, (a bisa saba masa) mafi kuma dauwama (a kan saba masa.)"
71. Sukace "Bazamu fifitaka a kan abinda yazo mana (nadaga hujjoji mabayyana a bisa gaskiyar Annabi Musa) ba, Mun rantse da Mahaliccinmu, yi abinda zaka yi, zaka ƙare wannan rayuwa ta duniya ne kawai.
72. " Haƙiƙa mu mun bada gaskiya da ubangijinmu donya gafarta mana kusakuranmu (na shirka da waninsa,) da abinda ka tilashe mu kansa (nadaga tsafi, muka koya, muka aikata.) Allah shine yafi ka (kyakkyawan sakamako in an bi shi) shine kuma yafi ka dauwamar (azaba in an sabe shi.)
73. (Ubangiji yace,) Haƙiƙa al'amarin duk wanda yazowa Ubangijinsa yana kafiri (kamar Fir'auna,) haƙiƙa jahannama ce ke gareshi, bazai mutur e a cikinta ba (balle ya huta,) bazai rayu (rayuwa da zata amfane shi) ba.
74. Wanda yazowa Ubangijinsa yana mumini kuwa Yakuma aikata ayyuka nagargaru waɗancananka darajoji maɗaukaka sun tabbata a garesu.
75. Aljannatai na tabbata, ƙoramu suna gudana ƙarƙashinsu, masu dauwama cikinta, wancananka shine samakakon wanda ya tsarkaka (daga zunubai.)

(FITAR BANI ISRA'ILA DAGA MISRA DA TAFIYAR FIR'AUNA SABODA NEMANSU)

وَلَقَدْ أَوْحَيْنَا إِلَىٰ مُوسَىٰ أَنِ اسْرِ بِعِبَادِے فَاضْرِبْ لَهُمْ طَرِيقًا
فِي الْبَحْرِ يَبَسًا لَا تَخَافُ دَرَكًا وَلَا تَخْشَىٰ ﴿76﴾ فَأَتْبَعَهُمْ فِرْعَوْنُ
بِجُنُودِهِۦ فَغَشِيَهُم مِّنَ الْيَمِّ مَا غَشِيَهُمْ وَأَضَلَّ فِرْعَوْنُ قَوْمَهُۥ
وَمَا هَدَىٰ ﴿77﴾ يَٰبَنِے إِسْرَآءِيلَ قَدْ أَنجَيْنَٰكُم مِّنْ عَدُوِّكُمْ وَوَٰعَدْنَٰكُمْ
جَانِبَ الطُّورِ الْأَيْمَنَ وَنَزَّلْنَا عَلَيْكُمُ الْمَنَّ وَالسَّلْوَىٰ ﴿78﴾
كُلُواْ مِن طَيِّبَٰتِ مَا رَزَقْنَٰكُمْ وَلَا تَطْغَوْاْ فِيهِ فَيَحِلَّ عَلَيْكُمْ
غَضَبِے وَمَن يَحْلِلْ عَلَيْهِ غَضَبِے فَقَدْ هَوَىٰ ﴿79﴾ وَإِنِّے لَغَفَّارٌ لِّمَن تَابَ
وَءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحًا ثُمَّ اهْتَدَىٰ ﴿80﴾ * وَمَا أَعْجَلَكَ عَن قَوْمِكَ
يَٰمُوسَىٰ ﴿81﴾ قَالَ هُمُ أُوْلَآءِ عَلَىٰ أَثَرِے وَعَجِلْتُ إِلَيْكَ رَبِّ لِتَرْضَىٰ ﴿82﴾
قَالَ فَإِنَّا قَدْ فَتَنَّا قَوْمَكَ مِنۢ بَعْدِكَ وَأَضَلَّهُمُ السَّامِرِيُّ ﴿83﴾
فَرَجَعَ مُوسَىٰ إِلَىٰ قَوْمِهِۦ غَضْبَٰنَ أَسِفًا ﴿84﴾ قَالَ يَٰقَوْمِ
أَلَمْ يَعِدْكُمْ رَبُّكُمْ وَعْدًا حَسَنًا أَفَطَالَ عَلَيْكُمُ الْعَهْدُ
أَمْ أَرَدتُّمْ أَن يَحِلَّ عَلَيْكُمْ غَضَبٌ مِّن رَّبِّكُمْ فَأَخْلَفْتُم مَّوْعِدِے ﴿85﴾
قَالُواْ مَا أَخْلَفْنَا مَوْعِدَكَ بِمَلْكِنَا وَلَٰكِنَّا حُمِّلْنَا أَوْزَارًا
مِّن زِينَةِ الْقَوْمِ فَقَذَفْنَٰهَا فَكَذَٰلِكَ أَلْقَى السَّامِرِيُّ ﴿86﴾

ربع

76. Haƙiƙa mun aiko izuwa Annabi Musa, Kafita da bayina da dare (daga ƙasar Misra,) sanya hanya a cikin kogi ƙeƙashashshiya (a garesu, ta wajen duka da sandarka, saiya aikata abinda aka umarce shi dashi, sai Allah ya ƙeƙasar musu da ƙasar suka wuce a cikinta, wato daya doki kogi saiya dare kashi goma sha biyu). Kada kaji tsoron riska (ta Fir'auna) kada kaji tsoron nitsewa.
77. Fir'auna yabisu da rundinarsa (alhali yana taredasu,) abinda ya zaike musu (nadaga kogi) ya zaike musu (ya nutsar dasu,) Fir'auna ya ɓatar da mutanensa (da kiransu izuwa bauta masa) bai shiryesu saiya aukaddasu cikin halaka (sabanin fadinsa bana shiriyar daku ,sai hanyar shiriya.
78. Yaku Bani-Isra'ila, Mun tserar daku ,daga magaucinku (Fir'auna) mun nutsar dashi, munyi muku alƙawarin gefen dutse na dama, (zamu baiwa Annabi Musa alaihissalam Attaura don kuyi aiki da ita,) Mun saukar da darɓa da danshila a gareku (waɗanda aka samesu akwai Yahudu na zamanin Annabi Sallallahu alaihi wasallama, an goranta musu abinda Allah ya ni'imta kakanninsu dashi a zamanin Annabin Musa alaihissalam don shinfiɗa ga faɗin Ubangiji garesu.)
79. Kuci daga daɗaɗan abinda muka azurta muku, kada kuyi shisshigi (cikinsa da butilcewar ni'imar da akayi muku,) sai fishina ya sauka a gareku wanda fishina ya sauka a gareshi haƙiƙa ya zunduma a cikin wuta.
80. Haƙiƙa ni mai yawan gafara ne ga wanda ya tuba (daga shirka) ya bada gaskiya (da kaɗaita Allah,) yayi aiki nagari, (farilla da nafila) sannan ya shiriya (da zarcewa a kan abinda aka faɗahar izuwa mutuwarsa.)

(BAUTAR DAN MARAKI GUN BANI- ISRA'ILA)

81. Menene ya gaggautar dakai ga buran mutanenka (na wajen zuwan Mi'adin karɓar Attaura,) Ya Musa (alaika salamum?)
82. Yace, "Su waɗannan, gasu kusa dani suna tafe a bisa gurbina, nayi gaggawa ne izuwa gareka Ya Ubangiji donka yarda dani. (ya faɗi wannan ne saboda zaton zasu zoda gaggawa, sai kuma sukayi jinkiri". Sai Ubangiji yace;)
83. " Haƙiƙa mu, mun jarrabi mutanenka bayanka Samiri ya halakar dasu (suka bautawa dan maraƙi")
84. Annabi Musa (Alaihissalam) yakomo izuwa mutanensa yana mai fishi (dasu) mai tsananin ɓakin ciki, yace, "Yaku mutanena Ubangijinku bai muku alƙawari kyakkyawa bane (na gaskiya, cewa zai baku Attaura.)
85. Shin! Muddar rabuwatadaku ,ne tayi tsawo gareku, ko kun nufi fishiya sauka a kanku daga Ubangijinku, (saboda bautar ɗan maraƙi,) saboda haka kuka saba alƙawarina, (kuka ƙi zuwa a bayana?")
86. Sai Sukace, "Bamu saɓa alƙawarinka da ikonmu ba, sai dai mu an ɗora mana nauyenauye ne na adon mutanen Fir'auna (Bani-Isra'ila suka aro daga gunsu, sabodaza suyi wani biki ta zauna gunsu, sai muka jefa ta (a cikin wuta yayin da Samiri yayi umarni da haka,) To, kamar yadda muka jefa shima Samiri ya jefa (abinda yake tare dashi nadaga ƙereƙeren da kuma turɓaya wacce Samiri ya damƙeta daga gurbin kofaton godiyar Mala'ika Jibrilu alaihissalam) Sai yafito musu da ɗan maraƙi, gangar jiki naman dajini, yanata gunji (da ake jinsa, saboda turɓaya wacce tasirin rayuwa ya shiga ciki.) Sai Samiri da mutanensa sukace, Wannan shine ubangijinku ubangijin Annabi Musa alaihissalam, ya mance.

فَأَخْرَجَ لَهُمْ عِجْلًا جَسَدًا لَّهُۥ خُوَارٌ فَقَالُواْ هَٰذَآ إِلَٰهُكُمْ وَإِلَٰهُ مُوسَىٰ
فَنَسِيَ ﴿٨٧﴾ أَفَلَا يَرَوْنَ أَلَّا يَرْجِعُ إِلَيْهِمْ قَوْلًا وَلَا يَمْلِكُ لَهُمْ ضَرًّا
وَلَا نَفْعًا ﴿٨٨﴾ وَلَقَدْ قَالَ لَهُمْ هَٰرُونُ مِن قَبْلُ يَٰقَوْمِ إِنَّمَا فُتِنتُم بِهِۦ
وَإِنَّ رَبَّكُمُ الرَّحْمَٰنُ فَاتَّبِعُونِي وَأَطِيعُواْ أَمْرِي ﴿٨٩﴾ قَالُواْ لَن نَّبْرَحَ
عَلَيْهِ عَٰكِفِينَ حَتَّىٰ يَرْجِعَ إِلَيْنَا مُوسَىٰ ﴿٩٠﴾ قَالَ
يَٰهَٰرُونُ مَا مَنَعَكَ إِذْ رَأَيْتَهُمْ ضَلُّوٓاْ أَلَّا تَتَّبِعَنِ
أَفَعَصَيْتَ أَمْرِي ﴿٩١﴾ قَالَ يَبْنَؤُمَّ لَا تَأْخُذْ بِلِحْيَتِي وَلَا بِرَأْسِي
إِنِّي خَشِيتُ أَن تَقُولَ فَرَّقْتَ بَيْنَ بَنِي إِسْرَٰٓءِيلَ وَلَمْ تَرْقُبْ
قَوْلِي ﴿٩٢﴾ ۞ قَالَ فَمَا خَطْبُكَ يَٰسَٰمِرِيُّ ﴿٩٣﴾ قَالَ
بَصُرْتُ بِمَا لَمْ يَبْصُرُواْ بِهِۦ فَقَبَضْتُ قَبْضَةً مِّنْ أَثَرِ
الرَّسُولِ فَنَبَذْتُهَا وَكَذَٰلِكَ سَوَّلَتْ لِي نَفْسِي ﴿٩٤﴾ قَالَ فَاذْهَبْ
فَإِنَّ لَكَ فِي الْحَيَوٰةِ أَن تَقُولَ لَا مِسَاسَ وَإِنَّ لَكَ
مَوْعِدًا لَّن تُخْلَفَهُۥ وَانظُرْ إِلَىٰٓ إِلَٰهِكَ الَّذِي ظَلْتَ
عَلَيْهِ عَاكِفًا لَّنُحَرِّقَنَّهُۥ ثُمَّ لَنَنسِفَنَّهُۥ فِي الْيَمِّ نَسْفًا ﴿٩٥﴾
إِنَّمَآ إِلَٰهُكُمُ اللَّهُ الَّذِي لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَسِعَ كُلَّ شَيْءٍ عِلْمًا ﴿٩٦﴾

ثمن

87. (Sai Ubangiji yace) "Yanzu basa ganin baya juyar da magana izuwa garesu (shi wannan đan maraƙi?)
88. "Bai mallaki cuta a garesu ba wala amfani."
89. Haƙiƙa Annabi Haruna (alaihissalam) yace musu tun kafin Annabi Musa bai komo ba, (Yace,) "Yaku mutanena haƙiƙa an jarrabe kune dashi, haƙiƙa Ubangijinku dai Arrhamanu ne, kubini (a cikin bauta tasa kubi) umarnina (a cikinta.')
90. Sai Sukace, "Mu bazamu gushe masu dukufa a kan bauta masa ba har sai Annabi Musa yakomo izuwa garemu".
91. (Annabi Musa) yace, (musu bayan komowarsa) "Ya Harunu me ya hanaka yayin daka gansu sun ɓata kabini? Shin ka saɓi umarnina ne (saboda zamanka a tsakanin wađanda suke bautawa wanin Allah?)"
92. Annabi Haruna yace, "Ya kai đan đan'uwata kada kayi riƙo da gemuna (alhali ya damƙa gemunsa da hannun hagu) wala da kaina (ya kasance ya riƙi gashinsa da hannun dama don fishi, ni naji tsoro dana bika lallai wađansu mutane daga wađanda basu bauta đan- maraƙi bazasu bini,) naji tsoron kace na rarraba tsakanin Bani-Isra'ila bakayi sauraron maganataba."
93. Sai yace, Menene sha'aninka ne wanda ya kira ka izuwa abinda ka aikatan nan ya Samiri?"
94. Yace, "Na lurane da abinda basu lura dashi ba saina đauki danƙi daga turɓayar gurbin kofaton gođiyar Mala'ika Jibrila, saina watsata a cikin surar đan - maraƙin wanda aka ƙera, hakana kaina ta ƙawata mini".
95. Sai Annabi Musa yace (dashi) "Tafi (daga tsakaninmu,) yana gareka muddin rayuwarka ka dinga cewa karka kusance ni" (To, ya kasance yana nausawa a cikin daji idan ya taɓa wani ko wani ya taɓashi duk saisu kamu da ciwo,) haƙiƙa kana da alkawari (na azabarka) bazaka saɓashi ba, sai kayi duba izuwa ubangijinka daka duƙufa kana bauta a gareshi, lallai zamu ƙone shi da wuta sannan zamu sheƙe shi a cikin zurfin kogi sheƙewa.
96. " Haƙiƙa Ubangijinku Allah ne kađai, Ubangijinku wanda ba abin bautawa da gaskiya sai shi, iliminsa ya yalwaci komai.'

كَذَٰلِكَ نَقُصُّ عَلَيْكَ مِنْ أَنۢبَآءِ مَا قَدْ سَبَقَ ۚ وَقَدْ ءَاتَيْنَٰكَ
مِن لَّدُنَّا ذِكْرًا ﴿99﴾ مَّنْ أَعْرَضَ عَنْهُ فَإِنَّهُۥ يَحْمِلُ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ
وِزْرًا ﴿100﴾ خَٰلِدِينَ فِيهِ ۖ وَسَآءَ لَهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ حِمْلًا ﴿101﴾
يَوْمَ يُنفَخُ فِى ٱلصُّورِ ۚ وَنَحْشُرُ ٱلْمُجْرِمِينَ يَوْمَئِذٍ زُرْقًا ﴿102﴾
يَتَخَٰفَتُونَ بَيْنَهُمْ إِن لَّبِثْتُمْ إِلَّا عَشْرًا ﴿103﴾ نَّحْنُ أَعْلَمُ
بِمَا يَقُولُونَ إِذْ يَقُولُ أَمْثَلُهُمْ طَرِيقَةً إِن لَّبِثْتُمْ إِلَّا يَوْمًا ﴿104﴾
وَيَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلْجِبَالِ فَقُلْ يَنسِفُهَا رَبِّى نَسْفًا ﴿105﴾ فَيَذَرُهَا قَاعًا
صَفْصَفًا ﴿106﴾ لَّا تَرَىٰ فِيهَا عِوَجًا وَلَآ أَمْتًا ﴿107﴾ يَوْمَئِذٍ يَتَّبِعُونَ
ٱلدَّاعِىَ لَا عِوَجَ لَهُۥ ۖ وَخَشَعَتِ ٱلْأَصْوَاتُ لِلرَّحْمَٰنِ فَلَا تَسْمَعُ إِلَّا هَمْسًا ﴿108﴾
يَوْمَئِذٍ لَّا تَنفَعُ ٱلشَّفَٰعَةُ إِلَّا مَنْ أَذِنَ لَهُ ٱلرَّحْمَٰنُ وَرَضِىَ لَهُۥ قَوْلًا ﴿109﴾
يَعْلَمُ مَا بَيْنَ أَيْدِيهِمْ وَمَا خَلْفَهُمْ وَلَا يُحِيطُونَ بِهِۦ عِلْمًا ﴿110﴾
۞ وَعَنَتِ ٱلْوُجُوهُ لِلْحَىِّ ٱلْقَيُّومِ ۖ وَقَدْ خَابَ مَنْ حَمَلَ ظُلْمًا ﴿111﴾ ربع
وَمَن يَعْمَلْ مِنَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَلَا يَخَافُ ظُلْمًا
وَلَا هَضْمًا ﴿112﴾ وَكَذَٰلِكَ أَنزَلْنَٰهُ قُرْءَانًا عَرَبِيًّا وَصَرَّفْنَا
فِيهِ مِنَ ٱلْوَعِيدِ لَعَلَّهُمْ يَتَّقُونَ أَوْ يُحْدِثُ لَهُمْ ذِكْرًا ﴿113﴾

(MASU BUJIREWA GA BURAN ALƘUR'ANI RANAR ALƘIYAMA)

97. Tamfar da muka labarta wannan ƙissa gareka (Ya Annabi Muhammadu Sallallahu alaika wasallama) muke labartawa daga labarun al'uma data gabata a gareka, haƙiƙa mun baka Alƙur'ani daga garemu.

98. Wanda ya bijire ga buransa (bai bada gaskiya dashi ba) haƙiƙa shi zai ɗauki jinkirarren kaya (na zunubi) a ranar Alƙiyama.

99. Masu dauwama a cikinsa, ya munana kayagaresu ranar alƙiyama.

100. Ranar da ake busa a cikin ƙaho, busa ta biyu, muna tara kafirai a wannan rana suna masu jan ido da baƙar fuska.

101. Suna asirtawa tsakaninsu cewa baku zauna (a duniya) ba sai kwana goma.

102. Mune masana da abinda suka faɗa a cikin wannan, (wato yadda suka faɗa ba haka ne ba) yayin da mafi adalcinsu hanya yake faɗa, baku zauna ba sai wuni ɗaya. (saboda abinda suke ganinsa a lahira na tsamakatai.

103. Suna tambayarka ga duwarwatsu, yaya zasu kasance ranar alƙiyama, cene (dasu) "Ubangijina zai sheƙeta sheƙewa (ya ɗaiɗaita tada iskoki.)

104. "Ya maida ita fuskar ƙasa madaidaici ya bazaka ga kwari cikinta ba wala tudu.

105. "A wannan rana mutane suke bin mai kira (izuwa tashin alƙiyama bayan tashinsu daga kabamruka, shine Mala'ika Israfilu alaihissalam, zaice Kuzo izuwa bijirarwar Ubangiji) babu karkacewa gareshi, muryoyi za suyi ƙas saboda Ubangiji Arrahmanu, baka jin komai sai motsin sawaye.

106. Rannadda ceto ɓata amfanin kowa, sai wanda Sarki Arrahman yayi wa izini yayi ceto, ya yarda da maganarsa, (shine ya fadi La'ilaha Illallahu, wato sai masu yawaitawa da ambaton Allah a nan duniya.)

107. Yasan abinda yake gabansu (na daga alamarin lahira) da abinda yake bayansu (nadaga al'amarin duniya,) basu kewaye sani da wannan ba.

108. Duka fuskoki sun tursasa ga Sarki rayayye wanda ya tokare sammai da ƙassai, haƙiƙa wanda ya aikata zalunci (shine mishrikanci) ya taɓe.

109. Duka wanda ya aikata daga aiyuka nagari alhali yana mumini bazai ji tsoron zalunci (na kari a cikin sayyi'a tasa) bako gurmitsewa (da tauyewa a cikin hasana tasa) ba.

110. Misalin yadda muka saukar da abinda aka ambata, hakana muka saukar da Alƙur'ani Balarabe, muka maimaita a cikinsa nagargaɗi, donsuji tsoron Allah, ko ya farar musu da gargadi.

فَتَعَٰلَى ٱللَّهُ ٱلْمَلِكُ ٱلْحَقُّ وَلَا تَعْجَلْ بِٱلْقُرْءَانِ مِن قَبْلِ
أَن يُقْضَىٰ إِلَيْكَ وَحْيُهُۥ وَقُل رَّبِّ زِدْنِى عِلْمًا ﴿111﴾ وَلَقَدْ
عَهِدْنَا إِلَىٰ ءَادَمَ مِن قَبْلُ فَنَسِىَ وَلَمْ نَجِدْ لَهُۥ عَزْمًا ﴿112﴾
وَإِذْ قُلْنَا لِلْمَلَٰٓئِكَةِ ٱسْجُدُوا لِءَادَمَ فَسَجَدُوا إِلَّا إِبْلِيسَ أَبَىٰ ﴿113﴾
فَقُلْنَا يَٰٓـَٔادَمُ إِنَّ هَٰذَا عَدُوٌّ لَّكَ وَلِزَوْجِكَ فَلَا يُخْرِجَنَّكُمَا
مِنَ ٱلْجَنَّةِ فَتَشْقَىٰٓ ﴿114﴾ إِنَّ لَكَ أَلَّا تَجُوعَ فِيهَا وَلَا تَعْرَىٰ ﴿115﴾
وَإِنَّكَ لَا تَظْمَؤُا فِيهَا وَلَا تَضْحَىٰ ﴿116﴾ فَوَسْوَسَ
إِلَيْهِ ٱلشَّيْطَٰنُ قَالَ يَٰٓـَٔادَمُ هَلْ أَدُلُّكَ عَلَىٰ شَجَرَةِ
ٱلْخُلْدِ وَمُلْكٍ لَّا يَبْلَىٰ ﴿117﴾ فَأَكَلَا مِنْهَا فَبَدَتْ لَهُمَا
سَوْءَٰتُهُمَا وَطَفِقَا يَخْصِفَانِ عَلَيْهِمَا مِن وَرَقِ ٱلْجَنَّةِ
وَعَصَىٰٓ ءَادَمُ رَبَّهُۥ فَغَوَىٰ ﴿118﴾ ثُمَّ ٱجْتَبَٰهُ رَبُّهُۥ فَتَابَ عَلَيْهِ وَهَدَىٰ ﴿119﴾
قَالَ ٱهْبِطَا مِنْهَا جَمِيعًا بَعْضُكُمْ لِبَعْضٍ عَدُوٌّ فَإِمَّا يَأْتِيَنَّكُم
مِّنِّى هُدًى ﴿120﴾ فَمَنِ ٱتَّبَعَ هُدَاىَ فَلَا يَضِلُّ وَلَا يَشْقَىٰ ﴿121﴾ وَمَنْ أَعْرَضَ
عَن ذِكْرِى فَإِنَّ لَهُۥ مَعِيشَةً ضَنكًا وَنَحْشُرُهُۥ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ أَعْمَىٰ ﴿122﴾
قَالَ رَبِّ لِمَ حَشَرْتَنِىٓ أَعْمَىٰ وَقَدْ كُنتُ بَصِيرًا ﴿123﴾

111. Hak̃ik̃a Sarki matabbaci ya girmama (ga buran abinda mushrikai suke fada,) kada kayi garaje da karatun Alk̃ur'ani tun gaban Jibrilu bai gama maka sak̃onsa ba, kace "Ubangijina k̃areni ilimi.

(ƘISSAR SAJADA GA ANNABI ADAMU ALAIHISSALA) WACCE TA ƘUNSHI SHUUMIN SABON ALLAH. ALLAH KIYA SHEMU)

112. Hak̃ik̃a munyi alk̃awari izuwa Annabi Adam (mukayi masa wasiyya da kada yaci itaciya tun gaban baici ba,) yabar wasiyyar tamu bai sami dauriya (ga barin abinda muka hane shi ga buransa) ba.
113. Ka ambata zamanin da muka fad̃a ga Mala'iku, "Kuyi sajada ga Annabi Adam (alaihissalam) sukayi sajada sai Iblis shine uban aljannu (ya kasance yana abutar Mala'iku yana bautawa Allah tare dasu) Yak̃i yin (sajada ga Annabi Adamu yace nine mafifici daga gareshi.)
114. Sai mukace ya Adamu hak̃ik̃a wannan magaucinka ne magaucin matarka ne (Hauwa'u) kada ya fitar daku ,daga aljanna ku fad̃a cikin wahala, (kayi noma, kayi shuka, kayi girbi, kayi nik̃a ka kwaba gurasa.
115. Hak̃ik̃a bazaka yunwata ba a cikinta baza kayi tsiraici ba.
116. Hak̃ik̃a kai bazakaji k̃ishirwa a cikinta ba, bazaka shiga rana ba.
117. Sai shaid̃an yayi waswasi gareshi yace, "Ya Adamu shin bana shiryar dakai bane a kan itaciyar dauwama (wacce wanda yaci ta yake dauwama) da mulki wanda bazai kare ba (bazai tsufa ba?)"
118. Sai Annabi Adamu da Hauwa'u sukaci daga itaciyar nan, sai tsiraikainsu ya bayyana a garesu (kowa yaga kowa, suka had̃u suna bankewa a kansu daga ganyen aljanna, saboda suyi suttura dashi,) Annabi Adamu ya aikata aiki mai kamar sab̃o ga ubangijinsa, saboda haka ya b̃acewa (muradinsa.)
119. Sannan Ubangijinsa ya zab̃eshi Yakusanta shiya karb̃i tubansa ya shirye shi izuwa dauwama kan tuba.
120. Yace, "Ku sauka (Yaku adamu da Hauwa'u tareda abinda kuka kunsa tareda zuriyyarku daga aljanna) baki d̃aya, ba'alinku mai k̃iyayya ne ga ba'ali, to, idan shiriya tazo muku daga gareshi.
121. To wanda yabi shiriyata shine alk̃ur'ani to bazai b̃ata a duniyaba bazai wahala a lahira ba.
122. "Wanda ya bijire ga buran Alk̃ur'anina bai gasgata dashi ba, to, hak̃ik̃a wannan mutum yana da rayuwa k̃unk̃unta (shine azaba a k̃abarinsa) zamu tara shi ranar alk̃iyama yana makaho.
123. Yace, "Ubangijina! Donme ka tashe ni ina makaho alhali ni mai ganine (a duniya?)"

قَالَ كَذَٰلِكَ أَتَتْكَ ءَايَٰتُنَا فَنَسِيتَهَا وَكَذَٰلِكَ اَ۬لْيَوْمَ تُنسَىٰ ﴿124﴾
وَكَذَٰلِكَ نَجْزِے مَنْ أَسْرَفَ وَلَمْ يُؤْمِنۢ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِۦ وَلَعَذَابُ اُ۬لْأٓخِرَةِ
أَشَدُّ وَأَبْقَىٰٓ ﴿125﴾ * أَفَلَمْ يَهْدِ لَهُمْ كَمْ أَهْلَكْنَا قَبْلَهُم مِّنَ اَ۬لْقُرُونِ
يَمْشُونَ فِے مَسَٰكِنِهِمْ إِنَّ فِے ذَٰلِكَ ءَلَأٓيَٰتٍ لِّأُوْلِے اِ۬لنُّهَىٰ ﴿126﴾
وَلَوْلَا كَلِمَةٌ سَبَقَتْ مِن رَّبِّكَ لَكَانَ لِزَامًا وَأَجَلٌ مُّسَمًّى ﴿127﴾
فَاصْبِرْ عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَسَبِّحْ بِحَمْدِ رَبِّكَ قَبْلَ طُلُوعِ اِ۬لشَّمْسِ وَقَبْلَ غُرُوبِهَا
وَمِنْ ءَانَآءِ اِ۬ليْلِ فَسَبِّحْ وَأَطْرَافَ اَ۬لنَّهَارِ لَعَلَّكَ تَرْضَىٰ ﴿128﴾
وَلَا تَمُدَّنَّ عَيْنَيْكَ إِلَىٰ مَا مَتَّعْنَا بِهِۦٓ أَزْوَٰجًا مِّنْهُمْ زَهْرَةَ اَ۬لْحَيَوٰةِ اِ۬لدُّنْيَا ﴿129﴾
لِنَفْتِنَهُمْ فِيهِ وَرِزْقُ رَبِّكَ خَيْرٌ وَأَبْقَىٰ ﴿130﴾ وَأْمُرْ أَهْلَكَ بِالصَّلَوٰةِ
وَاصْطَبِرْ عَلَيْهَا لَا نَسْـَٔلُكَ رِزْقًا نَّحْنُ نَرْزُقُكَ وَالْعَٰقِبَةُ
لِلتَّقْوَىٰ ﴿131﴾ وَقَالُواْ لَوْلَا يَأْتِينَا بِـَٔايَةٍ مِّن رَّبِّهِۦٓ أَوَلَمْ تَأْتِهِم
بَيِّنَةُ مَا فِے اِ۬لصُّحُفِ اِ۬لْأُولَىٰ ﴿132﴾ وَلَوْ أَنَّآ أَهْلَكْنَٰهُم بِعَذَابٍ
مِّن قَبْلِهِۦ لَقَالُواْ رَبَّنَا لَوْلَا أَرْسَلْتَ إِلَيْنَا رَسُولًا فَنَتَّبِعَ ءَايَٰتِكَ
مِن قَبْلِ أَن نَّذِلَّ وَنَخْزَىٰ ﴿133﴾ قُلْ كُلٌّ مُّتَرَبِّصٌ فَتَرَبَّصُواْ
فَسَتَعْلَمُونَ مَنْ أَصْحَٰبُ اُ۬لصِّرَٰطِ اِ۬لسَّوِيِّ وَمَنِ اِ۪هْتَدَىٰ ﴿134﴾

ثمن

124. Yace, "al'amarin haka yake, haƙiƙa ayoyinmu sun zo maka kayi burus da ita hakana yau za ayi buris dakai."

125. Hakana irin yadda muka sakawa wanda yayi shirka bai bada gaskiya da ayoyin Ubangijinsa ba, haƙiƙa azabar lahira tafi tsanani (daga azabar duniya data kabari) tafi dauwama.

(IZNACE-IZNACE DA NASIHOHI)

126. Shin bai bayyana ga kafirai bane nawa nawa muka halakar gabansu daga tsaraiku, suna tafiya a gidaddajinsu (a cikin tafiye-tafiyensu izuwa Sham, da waninta suyi izna,) haƙiƙa akwai iznace-iznace a cikin wancananka ga ma'abuta hankula.

127. Ba don kalmar data rigaya daga Ubangijinka (da jinkirin azaba izuwa ranar Lahiraba) da halakar dasu a nan duniyaya zama tilas, da ajali abin sanyawa garesu.

128. To, sai ka haƙura a bisa abinda suke faɗa (ayar kisa ta shafe wannan) kayi salla tareda godiyar ubangijinka, gaban hudowar rana (wato sallar asuba) da gaban faɗuwarta (sallar la'asar,) kayi salla daga sa'o'in ɗare, (sallar magaribada lisha) da gyaffen rana (sallar azahar domin lokacinta yana shigowa da zawalin rana ga buran tsatstsakin sama,) donka yarda da abindaza a baka na sakamako.

129. Kadaka miƙa idandunanka izuwa abinda muka jiyar da nau'o'in daga garesu daɗi dashi, na ƙyalƙyalin rayuwar duniya.

130. Donmu futincesu a cikinsa saboda (su tsaga) arzikin ubangijinka (a cikin aljanna) shine yafi (daga abinda aka basu a duniya) shine yafi dauwama.

MUHIMMANCIN SALLAH DA UMARNIN IYALI DA ITA

131. Ka umarci iyalinka da salla, ka daure a kanta, bamu kallafa maka azurtawa (ga kanka ko waninka) ba, mune masu azurtaka (haka waninka) kyakkyawan ƙarshe ya tabbata ga masu tsoron Allah.

132. Sai mushrikai Sukace, "Donme (Annabi Muhammadu Salallahu alaihi wasallama) baizo mana da ayoyi daga Ubangijinsa ba (daga abinda suka ƙago?) Shin bayanin abinda yake littattafan farko baizo musu bane (na daga labarun al'ummar da suka wuce da halakar dasu saboda ƙaryata manzanni...)

133. Da haƙiƙa mu mun halakar dasu da azaba gaban Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) da (a ranar Lahira) sai suce, "Ubangiji donme baka aiko jakada izuwa garemu ba, mubi ayoyinka (wandaka aiko da ita) tun gaban bamu wulaƙantu (a lahira) bamuji kunya (a cikin jahannama) ba".

134. Cene (dasu) "Kowanne (damu daku) mai sauraron (al'amarinsa) ne, to, kuyi sauraro da sannu kwa sani (a ranar Lahira) suwaye mazowa tafarki madaidaici, suwaye suka shiriya (daga waɗanda suka ɓata mu koku.)

21 سُورَةُ الأَنبِيَاءِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ مِائَةٌ وَإِحْدَىٰ عَشْرَةَ آيَة 111

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

حزب

* اقْتَرَبَ لِلنَّاسِ حِسَابُهُمْ وَهُمْ فِي غَفْلَةٍ مُّعْرِضُونَ ﴿1﴾ مَا يَأْتِيهِم
مِّن ذِكْرٍ مِّن رَّبِّهِم مُّحْدَثٍ إِلَّا اسْتَمَعُوهُ وَهُمْ يَلْعَبُونَ ﴿2﴾
لَاهِيَةً قُلُوبُهُمْ وَأَسَرُّوا النَّجْوَى الَّذِينَ ظَلَمُوا هَلْ هَٰذَا إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ
أَفَتَأْتُونَ السِّحْرَ وَأَنتُمْ تُبْصِرُونَ ﴿3﴾ قَالَ رَبِّي يَعْلَمُ الْقَوْلَ
فِي السَّمَاءِ وَالْأَرْضِ وَهُوَ السَّمِيعُ الْعَلِيمُ ﴿4﴾ بَلْ قَالُوا أَضْغَاثُ
أَحْلَامٍ بَلِ افْتَرَاهُ بَلْ هُوَ شَاعِرٌ فَلْيَأْتِنَا بِآيَةٍ كَمَا أُرْسِلَ
الْأَوَّلُونَ ﴿5﴾ مَا آمَنَتْ قَبْلَهُم مِّن قَرْيَةٍ أَهْلَكْنَاهَا أَفَهُمْ
يُؤْمِنُونَ ﴿6﴾ وَمَا أَرْسَلْنَا قَبْلَكَ إِلَّا رِجَالًا نُّوحِي إِلَيْهِمْ
فَاسْأَلُوا أَهْلَ الذِّكْرِ إِن كُنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴿7﴾ وَمَا جَعَلْنَاهُمْ جَسَدًا
لَّا يَأْكُلُونَ الطَّعَامَ وَمَا كَانُوا خَالِدِينَ ﴿8﴾ ثُمَّ صَدَقْنَاهُمُ الْوَعْدَ
فَأَنجَيْنَاهُمْ وَمَن نَّشَاءُ وَأَهْلَكْنَا الْمُسْرِفِينَ ﴿9﴾ لَقَدْ
أَنزَلْنَا إِلَيْكُمْ كِتَابًا فِيهِ ذِكْرُكُمْ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿10﴾

وَكَمْ قَصَمْنَا

Suratul Anbiya'i Alaihimusalam

A Makka Aka Saukar Da Ita Ayoyinta Dari Da Goma Sha Daya (111)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

"Ita wannan sura tana kiran Mushrikai izuwa aƙidar Musulunci, tana gargaɗi da tsarmakatan ranar Lahira, tana nuna yadda Annabawa suka kirawo mutane da shan gwagwarmaya a cikin hanyarsu izuwa kiranye izuwa Ubangiji"

(MUSHRIKAI DA DA'AWARSU DA RADDI A KANSU)

1. Sakamakon mutane (shine ranar alƙiyama) Yakusanta ga mutane, (mutanen Makka masu musun tashin alƙiyama,) alhali su suna masu rafkana masu bijirewa (ga buran tanadi saboda ita).
2. Wani gargaɗi daga Ubangijinsu bazaizo musu ba face sun saurare shi alhali su suna izgili dashi.
3. Zukatansu suna marabkana ga buran ma'anarsa, waɗanda sukayi zalunci sun ɓoye ganawa, wannan (suna nufin Manzon Allah Salallahu alaihi wasallama) bai kasance ba face mutumne kamar ku (abinda yazo dashi tsafi ne,) donme kuke zuwa wa tsafi alhali ku kuna ganinsa (tsafi ne?)
4. Cene dasu Ubangijina yasan magana a cikin sama da ƙasa, shine ainihin maiji ga abinda suka ɓoye, masani dashi.
5. Bari! Sun faɗa (a cikin abinda yazo dashi na alƙur'ani, sun faɗa cewa abinda yazo dashi) cuɗanye-cuɗanye ne dayaganta a cikin barci, (sunce) "Kai, ƙirƙirar alƙur'ani yayi, kai shi mawaƙi ne, abinda yazo dashi waƙa ne. To, sai kazo mana da aya kamar yadda aka aikowa mutanen farko (kamar taguwa da sanda da hannu, Ubangiji yace:)
6. Babu wata alƙarya data bada gaskiyagabansu muka halakar da ita, (saboda ƙaryatawar abinda yazo mata na daga ayoyi, Shin,) to sune zasu bada gaskiya?
7. Bamu aiko daga gabanka ba face mutane da muke aikowa izuwa garesu (ba Mala'iku ba). Ku tambayi mazowa zikiri (wato malaman Attaura da Linjila) in kun kasance baku san (wannan ba, saboda su sun sanshi, ku kuma kunfi kusanci izuwa gasgata shi daga gasgatawar muminai da Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama.)

HALACCIN BUJERE BUJERE NA MUTUMTAKA GA MANZANNI ALAIHIMUSSALAMU

8. Bamu sanya manzanni jukkuna da basa cin abinci ba, (bari! suna cinsa), basu kasance masu dauwama a duniya ba.
9. Sannan muka gasgata musu alƙawari (da tserar dasu,) to, muka tserar dasu tareda wanda muka ga damar (tserar dashi,) muka halakar da mabarnata (masu ƙaryatawa garesu.)
10. Haƙiƙa mun saukar da littafi izuwa gareku (ku ƙuraishawa,) ambatonku (wato ɗaukakar ku) tana ciki (saboda da harshenku aka saukar dashi.) Shin, to, bakwayi hankali ba (ku bada gaskiya dashi?)

وَكَمْ قَصَمْنَا مِن قَرْيَةٍ كَانَتْ ظَالِمَةً وَأَنشَأْنَا بَعْدَهَا قَوْمًا ءَاخَرِينَ ﴿11﴾
فَلَمَّا أَحَسُّواْ بَأْسَنَا إِذَا هُم مِّنْهَا يَرْكُضُونَ ﴿12﴾ لَا تَرْكُضُواْ
وَارْجِعُواْ إِلَىٰ مَا أُتْرِفْتُمْ فِيهِ وَمَسَٰكِنِكُمْ لَعَلَّكُمْ تُسْـَٔلُونَ ﴿13﴾
قَالُواْ يَٰوَيْلَنَا إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ﴿14﴾ فَمَا زَالَت تِّلْكَ دَعْوَىٰهُمْ
حَتَّىٰ جَعَلْنَٰهُمْ حَصِيدًا خَٰمِدِينَ ﴿15﴾ * وَمَا خَلَقْنَا ٱلسَّمَآءَ
وَٱلْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا لَٰعِبِينَ ﴿16﴾ لَوْ أَرَدْنَا أَن نَّتَّخِذَ لَهْوًا
لَّاتَّخَذْنَٰهُ مِن لَّدُنَّا إِن كُنَّا فَٰعِلِينَ ﴿17﴾ بَلْ نَقْذِفُ بِالْحَقِّ عَلَى
ٱلْبَٰطِلِ فَيَدْمَغُهُۥ فَإِذَا هُوَ زَاهِقٌ وَلَكُمُ ٱلْوَيْلُ مِمَّا تَصِفُونَ ﴿18﴾
وَلَهُۥ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَنْ عِندَهُۥ لَا يَسْتَكْبِرُونَ
عَنْ عِبَادَتِهِۦ وَلَا يَسْتَحْسِرُونَ ﴿19﴾ يُسَبِّحُونَ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ
لَا يَفْتُرُونَ ﴿20﴾ أَمِ ٱتَّخَذُواْ ءَالِهَةً مِّنَ ٱلْأَرْضِ هُمْ يُنشِرُونَ ﴿21﴾
لَوْ كَانَ فِيهِمَا ءَالِهَةٌ إِلَّا ٱللَّهُ لَفَسَدَتَا فَسُبْحَٰنَ ٱللَّهِ رَبِّ ٱلْعَرْشِ
عَمَّا يَصِفُونَ ﴿22﴾ لَا يُسْـَٔلُ عَمَّا يَفْعَلُ وَهُمْ يُسْـَٔلُونَ ﴿23﴾ أَمِ ٱتَّخَذُواْ
مِن دُونِهِۦ ءَالِهَةً قُلْ هَاتُواْ بُرْهَٰنَكُمْ هَٰذَا ذِكْرُ مَن مَّعِيَ وَذِكْرُ
مَن قَبْلِي بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ٱلْحَقَّ فَهُم مُّعْرِضُونَ ﴿24﴾

ثمن

(BAN TSORO DA BARAZANA)

11. Dayawa muka halakar nadaga alƙaryu (wato mutanenta) data kasance kafira, muka fari mutane waɗansu dabam bayanta.
12. A yayin da sukayi hasashe da tsananin riƙonmu, sai gasu suna kirirrima da dawakansu daga gareta.
13. (Mala'iku sukace musu don izgili,) "Kada kuyi kirimma ku komo izuwa wadaƙarkuda gidaddajinku, don a dinga tambayanku (wani abu daga duniyarku kamar yadda kuka saɓa (wato banbaɗawa)."
14. Sukace, "Wo-o-ho! Ya halakarmu, haƙiƙa mu mun kasance azzalumai (saboda kafircin da muke)".
15. Wancananka basu gushe ba Itace da'awarsu (dasuke addu'a da ita suke maimaitata,) har muka mai dasu girbabbu, matattu a bice.
16. Bamu halicci sammai da ƙassaida abinda yake cikinsu don wasanni ba, (mun halicce sune donsu nuna mana kin ƙudirarmu, da amfanin bayinmu.)

(AMBATON MUKADDAMU DA TALI A ILMIN MANDIƘI

17. Da mun nufi mu riƙi wasanni (mace ko da) da mun riƙe shi daga garemu, daga Hurul -aini da Mala'iku (in mun kasance masu aikata (wancananka, sai dai mu bamu aikata wannan ba, Ashe bamu nufe shi ba.)
18. Bari! Munajifa da gaskiya (imani) a kan ƙarya (kafirci) saita ragwargwatse shi sai gashi balbaltacce. Ku kafiran Almasihu kuna da azaba mai tsanani daga abinda kuke sufanta (Allah da mace da ɗa.).
19. Abinda yake sammai da ƙassaina Allah ne (mallaka da halittada bauta,) to, waɗanda suke wurin Ubangiji (na daga Mala'ikuda Annabawa da shuhada'u da salihuna) basa girman -kai (ga buran bautar Allah, basa gajiya.)
20. Suna tasbihi dukkan dare da rana basa gajiya (ga buransa, wani mai shagalarwa baya shagalar dasu.) (1)
21. Bari! Sun riƙi iyayen giji ne daga ƙasashe (kamar dutse da zinare da azurfa,) su iyayen gijin nan suke raya matattu (a'a, ba wandazai zama Allah sai mai raya matattu.)
22. Da da akwai iyayen giji cikin sammai da ƙassai wanin Allah dasun ruguje (saboda samun hana juna a tsakaninsu, yayin ƙididdigar iyayen giji) Tsarki ya tabbata ga Allah Ubangijin al'arshi, ga buran abinda suke sufanta (Allah dashi na daga shariki da waninsa.)
23. Ba a tambayar sa ga abinda yake aikatawa sune ake tambayarsu (ga ayyukansu.)
24. Bari! Donme suka riƙi iyayen giji ba Allah ba, to, cene; Ku zoda hujjar ku (a kan wannan,) wannan gargaɗin al'ummar data ke taredani ne, (shine alƙur'ani,) kuma gargaɗi ne na waɗanda suke gabana (na daga al'umma shine Attaura da Injila da waninsu, ba inda aka samu cewa Allah yana da shariki.) Bari! yawaicinSudai basu san Allah ba, su masu bijirewa ne (ga buran duba mai sadawa izuwa saninsa.)

1) Haka Annadawa da shuhada'u da salihuna suke, da dalilin "Allazina fi salatihim da'imuna" - Sanajy -

وَمَا أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ مِن رَّسُولٍ إِلَّا يُوحَىٰ إِلَيْهِ أَنَّهُ لَا إِلَٰهَ
إِلَّا أَنَا فَاعْبُدُونِ ﴿25﴾ وَقَالُوا اتَّخَذَ الرَّحْمَٰنُ وَلَدًا سُبْحَانَهُ
بَلْ عِبَادٌ مُّكْرَمُونَ ﴿26﴾ لَا يَسْبِقُونَهُ بِالْقَوْلِ وَهُم بِأَمْرِهِ يَعْمَلُونَ ﴿27﴾
يَعْلَمُ مَا بَيْنَ أَيْدِيهِمْ وَمَا خَلْفَهُمْ وَلَا يَشْفَعُونَ إِلَّا لِمَنِ ارْتَضَىٰ
وَهُم مِّنْ خَشْيَتِهِ مُشْفِقُونَ ﴿28﴾ وَمَن يَقُلْ مِنْهُمْ إِنِّي إِلَٰهٌ مِّن دُونِهِ
فَذَٰلِكَ نَجْزِيهِ جَهَنَّمَ كَذَٰلِكَ نَجْزِي الظَّالِمِينَ ﴿29﴾
* أَوَلَمْ يَرَ الَّذِينَ كَفَرُوا أَنَّ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضَ كَانَتَا رَتْقًا ربع
فَفَتَقْنَاهُمَا وَجَعَلْنَا مِنَ الْمَاءِ كُلَّ شَيْءٍ حَيٍّ أَفَلَا يُؤْمِنُونَ ﴿30﴾
وَجَعَلْنَا فِي الْأَرْضِ رَوَاسِيَ أَن تَمِيدَ بِهِمْ وَجَعَلْنَا فِيهَا
فِجَاجًا سُبُلًا لَّعَلَّهُمْ يَهْتَدُونَ ﴿31﴾ وَجَعَلْنَا السَّمَاءَ سَقْفًا
مَّحْفُوظًا وَهُمْ عَنْ آيَاتِهَا مُعْرِضُونَ ﴿32﴾ وَهُوَ الَّذِي خَلَقَ
اللَّيْلَ وَالنَّهَارَ وَالشَّمْسَ وَالْقَمَرَ كُلٌّ فِي فَلَكٍ يَسْبَحُونَ ﴿33﴾
وَمَا جَعَلْنَا لِبَشَرٍ مِّن قَبْلِكَ الْخُلْدَ أَفَإِن مِّتَّ فَهُمُ
الْخَالِدُونَ ﴿34﴾ كُلُّ نَفْسٍ ذَائِقَةُ الْمَوْتِ وَنَبْلُوكُم
بِالشَّرِّ وَالْخَيْرِ فِتْنَةً وَإِلَيْنَا تُرْجَعُونَ ﴿35﴾

25. Bamu aiko manzo ba gabanka face ana aikowa gareshi cewa shi babu abin bautawa da gaskiya saini, to, ku kaɗaita ni,
26. Sukace, "Sarki Arrahmanu ya riƙi da daga Mala'iku", Tsarki ya tabbata gareshi Bari! Su bayine ababan girmamawa, (bauta kuwa tana kishiyantar haihuwa.)
27. Basa rigayarsa da magana, (basa magana sai bayan yayi magana,) su suna aiki da umarninsa ne kawai.
28. Yasan abinda yake gabansu, (abinda suka aikata) da abinda yake bayansu, (abinda suke aikatawa,) basa ceto sai ga wanda Allah ya yarda (su cece shi,) su a firgice suke saboda tsoron Allah.
29. Wanda yace daga cikinsu, "Ni ubangiji ne ba Allah ba" (wato Iblisu dayayi kira izuwa bautar kansa.) Wancananka zamu saka masa jahannama, hakana muke sakawa mushrikai.

(KAFA DALILAI DA HALITTA A BISA SAMUWAR UBANGIJI MADAUKAKIN SARKI)

30. Shin, waɗanda suka kafirta basu sani bane cewa sammai da ƙassai sun kasance tosassu, sai muka kece su (muka zamar da sama bakwai,muka zamar da ƙasa bakwai,) muka sa sama tana ruwa ƙasa tana fitar da tsiri, muka sanyakowane abu rayayye daga ainihin ruwa, (mai saukowa daga sama da mai ɓulɓulowa daga ƙasa, wato dukkan tsiri rayayye da waninsa ruwa ne sababin rayuwarsa,) To shin basu bada gaskiyabane (da kaɗaita ni?)
31. Muka sanya duwarwatsu matabbata a cikin ƙasa, don kadata karkata dasu, muka sanya tafarku [1] mayalwata a cikin duwarwatsun nan donsu shiriya izuwa manufansu a cikin tafiyetafiye
32. Muka sanya sama rufi ga ƙasa (wato kamar rufi ga ɗaki) abin kiyayewa (ga buran faɗowa.) Su masu bijirewa ne ga buran ayoyinmu, (rana, wata, taurari da waninsu, basa tunani cikinta balle susan mahaliccinsu babu abokin tarayya dashi.)
33. Shine wanda ya halicci dare da wuni da rana da wata, kowanne (daga waɗannan taurari) suna ninƙaya a cikin wani abu kewayayye da ake ce dashi FALAKI.

(WANI ABU NA DAGA MATSAYIN MUSHRIKAI TAREDA MA'AIKIN ALLAH SALALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

34. Bamu sanya dauwama ga wani mutum gabanka ba, Shin in ka mutu su dauwama zasuyi, (a'a, wannan ta sauka ne lokacin da kafirai sukace Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama da sannu zai mutu.)
35. Dukkan rai mai nunfasawa zata ɗanɗani mutuwa ne, munajarrabar kuda hairi da sharri (talauci da wadata, rashin lafiya da lafiya,) don jarraba, (mu gani kwa daure ku gode ko kuwa?) Izuwa garemu za a komo daku ,(saboda sakamako.)

1) Saboda waɗannan tafarku mayalwatada Ubangiji yasanya su mayalwata aka sami damar tafiya daga Makka zuwa Madina da sauran irinsu. A can asalinsu tsakanin kowacce hanya da 'yaruwarta dutse daya ne, sai Allah yasanya waɗannan hanyoyi don saduwa. - Sanajiy -

وَإِذَا رَءَاكَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِن يَتَّخِذُونَكَ إِلَّا هُزُؤًا
أَهَٰذَا ٱلَّذِي يَذْكُرُ ءَالِهَتَكُمْ وَهُم بِذِكْرِ ٱلرَّحْمَٰنِ
هُمْ كَٰفِرُونَ ﴿36﴾ خُلِقَ ٱلْإِنسَٰنُ مِنْ عَجَلٍ سَأُوْرِيكُمْ
ءَايَٰتِي فَلَا تَسْتَعْجِلُونِ ﴿37﴾ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلْوَعْدُ
إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿38﴾ لَوْ يَعْلَمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ حِينَ لَا يَكُفُّونَ
عَن وُجُوهِهِمُ ٱلنَّارَ وَلَا عَن ظُهُورِهِمْ وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ ﴿39﴾
بَلْ تَأْتِيهِم بَغْتَةً فَتَبْهَتُهُمْ فَلَا يَسْتَطِيعُونَ رَدَّهَا
وَلَا هُمْ يُنظَرُونَ ﴿40﴾ وَلَقَدُ ٱسْتُهْزِئَ بِرُسُلٍ مِّن قَبْلِكَ
فَحَاقَ بِٱلَّذِينَ سَخِرُواْ مِنْهُم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿41﴾
* قُلْ مَن يَكْلَؤُكُم بِٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ مِنَ ٱلرَّحْمَٰنِ ثمن
بَلْ هُمْ عَن ذِكْرِ رَبِّهِم مُّعْرِضُونَ ﴿42﴾ أَمْ لَهُمْ ءَالِهَةٌ
تَمْنَعُهُم مِّن دُونِنَا لَا يَسْتَطِيعُونَ نَصْرَ أَنفُسِهِمْ وَلَا هُم مِّنَّا
يُصْحَبُونَ ﴿43﴾ بَلْ مَتَّعْنَا هَٰٓؤُلَآءِ وَءَابَآءَهُمْ حَتَّىٰ طَالَ
عَلَيْهِمُ ٱلْعُمُرُ أَفَلَا يَرَوْنَ أَنَّا نَأْتِي ٱلْأَرْضَ
نَنقُصُهَا مِنْ أَطْرَافِهَا أَفَهُمُ ٱلْغَٰلِبُونَ ﴿44﴾

36. Idan wađanda suka kafirta suka ganka, basa riƙonka sai abin izgili (dashi, suna cewa) "Yanzu wannan shine wanda yake laifanta iyayen gijinku, su masu kafircewa ne da ambaton Ubangiji Arrahmanu (Don sunce basu sanshi ba. (A yayin da suka nemi garajen saukar azaba, sai Allah yace:)
37. An halicci mutum daga garaje, (ai saboda yawan garajensa a cikin halayensa ai kamar an halicce shine daga garajen,) da sannu zamu đanđana muku kuđa ta azabaku daina neman gaggawar (azaba, a cikinsa ya nuna musu kisa a Badar.)
38. Suna cewa, "Yaushe ne wannan alƙawarin (na tashin alƙiyama) in kun kasance masu gaskiya?
39. Da wađanda suka kafirta sunsan loton da bazasu ije wuta ga buran fuskokinsu ba wala ga buran bayansu, su baza a hana musu azabar Allah ba (a ranar Lahira, da basu fađi abinda suka fađan nan ba.
40. Kai! Bari! Alƙiyama za tazo musu bagatatan baraɓe ta firgita su, bazasu sami damar maida ita ba, baza ayi musu sauraro (donsuyi hanzari ko su tuba) ba.
41. Haƙiƙa an izgili da manzanni na daga gabanka, (ana rarrashin Ma'aiki ne sallallahu alaihi wasallama) sai abin nan dasuke izgili dashiya sauka ga wađanda sukayi izgili daga cikinsu, (shine azaba, hakana zai sauka ga wanda yayi izgili da kai.)

(BA MAI JUYARWA GA KADDARAR ALLAH MADAUKAKIN SARKI)

42. Cene (dasu) "Wanene mai kiyaye kuda dare da rana ga buran (azabar) Ubangiji (idan zaita saukar?" Babu!) Bari! Sudai masu bijirewa ne ga buran ambaton Ubangijiusu, (Alƙur'ani basa tunani a cikinsa.)
43. Shin suna da iyayen giji dasuke hana su ga abinda yake damun su bamu ba, su iyayen gijin nan basu da ikon taimakon kansu, saboda haka bazasu taimake su ba, su kuma kafiran nan bazasu iya tsarshe su daga azabarmu ba.
44. Bari! Munji da wađannan dađi ne dasu da iyayensu, (mun jiyar dasu dađi da abinda muka ni'imta a garesu,) har rai ya tsawaita a garesu (suka ruđu dashi.) Shin basa dubane cewa mu haƙiƙa muna nufin ƙasarsu, muna tauye ta daga gyaffenta (da buđe ta ga Annabi Sallallahu alaihi wasallama) Shin to, sune masu rinjaye? (A'a, sai Annabi da sahababbansa.)

قُلْ إِنَّمَآ أُنذِرُكُم بِالْوَحْيِ وَلَا يَسْمَعُ الصُّمُّ الدُّعَآءَ
إِذَا مَا يُنذَرُونَ ﴿45﴾ وَلَئِن مَّسَّتْهُمْ نَفْحَةٌ مِّنْ عَذَابِ رَبِّكَ
لَيَقُولُنَّ يَٰوَيْلَنَآ إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ﴿46﴾ وَنَضَعُ الْمَوَٰزِينَ
الْقِسْطَ لِيَوْمِ الْقِيَٰمَةِ فَلَا تُظْلَمُ نَفْسٌ شَيْـًٔا وَإِن كَانَ
مِثْقَالَ حَبَّةٍ مِّنْ خَرْدَلٍ أَتَيْنَا بِهَا وَكَفَىٰ بِنَا حَٰسِبِينَ ﴿47﴾
وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ الْفُرْقَانَ وَضِيَآءً وَذِكْرًا
لِّلْمُتَّقِينَ ﴿48﴾ الَّذِينَ يَخْشَوْنَ رَبَّهُم بِالْغَيْبِ وَهُم مِّنَ السَّاعَةِ
مُشْفِقُونَ ﴿49﴾ وَهَٰذَا ذِكْرٌ مُّبَارَكٌ أَنزَلْنَٰهُ أَفَأَنتُمْ لَهُۥ مُنكِرُونَ ﴿50﴾
* وَلَقَدْ ءَاتَيْنَآ إِبْرَٰهِيمَ رُشْدَهُۥ مِن قَبْلُ وَكُنَّا بِهِۦ عَٰلِمِينَ ﴿51﴾ ربع
إِذْ قَالَ لِأَبِيهِ وَقَوْمِهِۦ مَا هَٰذِهِ التَّمَاثِيلُ الَّتِيٓ أَنتُمْ لَهَا عَٰكِفُونَ ﴿52﴾
قَالُوا۟ وَجَدْنَآ ءَابَآءَنَا لَهَا عَٰبِدِينَ ﴿53﴾ قَالَ لَقَدْ كُنتُمْ أَنتُمْ
وَءَابَآؤُكُمْ فِي ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿54﴾ قَالُوٓا۟ أَجِئْتَنَا بِالْحَقِّ أَمْ أَنتَ
مِنَ اللَّٰعِبِينَ ﴿55﴾ قَالَ بَل رَّبُّكُمْ رَبُّ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ
الَّذِي فَطَرَهُنَّ وَأَنَا۠ عَلَىٰ ذَٰلِكُم مِّنَ الشَّٰهِدِينَ ﴿56﴾ وَتَاللَّهِ
لَأَكِيدَنَّ أَصْنَٰمَكُم بَعْدَ أَن تُوَلُّوا۟ مُدْبِرِينَ ﴿57﴾

45. Cene (dasu) "Ni kawai inayi muku gargaɗi ne da wahayi (daga Allah badaga katarnin kaina ba,) kurame basa jin kira idan ana gargaɗinsu (Don basa aiki da abinda sukeji na daga gargaɗi, saboda haka su kurame ne").
46. Haƙiƙa idan wata 'yar mashafiya ta azabata samesu daga Ubangijinka lallai zasu dinga cewa, "Wo-ho-ho ya halakarmu, haƙiƙa mun kasance azzalumai (da mushrikanci da ƙaryata Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama)".

(MA'AUNIN RANAR ALƘIYAMA DA ADALCIN ALLAH)

47. Muna sanya ma'aunai ma'abuta adalci a cikin ranar alƙiyama, baza a zalunci wata kai wani abu ba, (na tauye hasana ko karin sayyi'a,) idan aiki ya kasance misalin ƙwayar komayya zamu zoda ita. Mun isa masu ƙididdigewa (a cikin kowane abu.)

(ANNABI MUSA DA HARUNA ALAIHIMUSSALAMU) WANDA YAKUNSHI JAWO HANKALIN YAHUDU IZUWA BADA GASKIYA DA ALƘUR'ANI

48. Haƙiƙa mun baiwa Annabi Musa da Haruna (alaihimussalamu) Furƙani, (ai Attaura) mai bayyanewa (tsakanin ƙarya da gaskiya, da halas da haram) da haske da gargaɗi (a cikinta) ga masu tsoron Allah.
49. Waɗanda suke tsoron Ubangijinsu a fake (ga buran mutane,) su masu firgita ne daga tsarmakatan tashin alƙiyama.
50. Wannan (alƙur'ani) gargaɗi ne mai albarka, muka saukar dashi. Tur! Shin to, ku masu musune gareshi?

(WANI ABU NADAGA ƘISSAR ANNABI IBRAHIM ALAIHISSALAM)

51. Haƙiƙa mun baiwa Annabi Ibrahim (alaihissalam) shiriya tasa tun gaban balaga tasa, mun tabbata' masana dashi ai masana (da cewa shi matsantsancine ga wancananka.)
52. Yayin daya faɗa ga mahaifinsa da mutanensa "Menene waɗannan gumaka da kuka dukufa a kan bautar ta"
53. Sukace "Mu mun sami iyayenmune suna bauta mata, (mukayi koyi dasu.)"
54. Yace (dasu) "Lallai kun kasance kuda iyayenku cikin ɓata mabayyani".
55. Sukace, "Kazo mana da gaskiya ne a cikin faɗin wannan, koko kai kana daga masu wasanni (a cikinsa.)"
56. Yace "Ubangijinku shine Ubangijin sammai da ƙassai wanda ya ƙagesu (ba bisa wani misali daya rigaya ba) ni, ina masu shaidawa a kan abin nan dana faɗa.
57. "Manaƙi, Wallahi zan yiwa gumakanku ƙaƙƙarfan tanadi bayan kunjuya kuna masu bada baya".

فَجَعَلَهُمْ جُذَٰذاً اِلَّا كَبِيراً لَّهُمْ لَعَلَّهُمْ إِلَيْهِ يَرْجِعُونَ ﴿58﴾
قَالُواْ مَن فَعَلَ هَٰذَا بِـَٔالِهَتِنَا إِنَّهُ لَمِنَ اَلظَّٰلِمِينَ ﴿59﴾ قَالُواْ
سَمِعْنَا فَتىً يَذْكُرُهُمْ يُقَالُ لَهُ إِبْرَٰهِيمُ ﴿60﴾ قَالُواْ
فَأْتُواْ بِهِ عَلَىٰ أَعْيُنِ اِلنَّاسِ لَعَلَّهُمْ يَشْهَدُونَ ﴿61﴾ قَالُواْ
ءَآنتَ فَعَلْتَ هَٰذَا بِـَٔالِهَتِنَا يَٰإِبْرَٰهِيمُ ﴿62﴾ قَالَ
بَلْ فَعَلَهُ كَبِيرُهُمْ هَٰذَا فَسْـَٔلُوهُمْ إِن كَانُواْ يَنطِقُونَ ﴿63﴾
فَرَجَعُواْ إِلَىٰ أَنفُسِهِمْ فَقَالُواْ إِنَّكُمْ أَنتُمُ اُلظَّٰلِمُونَ ﴿64﴾
ثُمَّ نُكِسُواْ عَلَىٰ رُءُوسِهِمْ لَقَدْ عَلِمْتَ مَا هَٰٓؤُلَآءِ
يَنطِقُونَ ﴿65﴾ قَالَ أَفَتَعْبُدُونَ مِن دُونِ اِللَّهِ مَا لَا يَنفَعُكُمْ شَيْـٔاً
وَلَا يَضُرُّكُمْ أُفٍّ لَّكُمْ وَلِمَا تَعْبُدُونَ مِن دُونِ اِللَّهِ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿66﴾
قَالُواْ حَرِّقُوهُ وَانصُرُواْ ءَالِهَتَكُمْ إِن كُنتُمْ فَٰعِلِينَ ﴿67﴾
قُلْنَا يَٰنَارُ كُونِي بَرْداً وَسَلَٰماً عَلَىٰ إِبْرَٰهِيمَ ﴿68﴾ وَأَرَادُواْ
بِهِ كَيْداً فَجَعَلْنَٰهُمُ اُلْأَخْسَرِينَ ﴿69﴾ وَنَجَّيْنَٰهُ وَلُوطاً اِلَى
اَلْأَرْضِ اِلَّتِي بَٰرَكْنَا فِيهَا لِلْعَٰلَمِينَ ﴿70﴾ وَوَهَبْنَا لَهُ
إِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ نَافِلَةً وَكُلّاً جَعَلْنَا صَٰلِحِينَ ﴿71﴾

58. Sai yasanya su gutsatstsari (bayan sun tafi izuwa matattararsu ranar Idi,) sai babbansu (ya rataya masa gatari a wuyansa,) ko sa komo izuwa gareshi, (su ga abinda ya aikata ga waninsa).
59. Sukace (bayan komowarsu da ganinsu abinda ya aikata) "Wanda ya aikata wannan ga iyayen gijinmu, Haƙiƙa shi yana daga cikin azzalumai".
60. Sukace, (wato sashinsu yace da sashi) "Munji wani saurayi yana laifanta su anace dashi Ibrahim".
61. Sukace, (dashi) "Kuzo dashi bisa idandunan mutane ƙarara watakila sa shaida a kansa (cewa shine yayi)".
62. Sukace (dashi bayan an kawo shi,) "Shin kaine ka aikata wannan ga iyayen gijinmu Ya Ibrahim?".
63. Yace, (yana mai shiru ga buran aikinsa,) "Bari, babbansune ya aikata wannan, ku tambaye su (wanda ya aikata wannan, aiki) in sun kasance suna firici (sa gaya muku wanda ya aikata" yanayi musujirwaye ne da cewa gunki wanda akasan gajiyawarsa ga buran aiki bazai kasance Allah ba).
64. Suka koma izuwa kawukansu (da tunani) sukace (ga kawukansu,) Haƙiƙa ku kune azzalumai (dan kun bautawa wanda ba yafirici)."
65. Sannan aka koma dasu a kan kawukansu (izuwa kafircinsu, wato Allah ne yayi musu haka) sukace "Wallahi haƙiƙa kasan wanđannan basa magana (ya zaka umarcemu da tambayarsu)."
66. Sai yace, "To, saboda me kuke bautawa ba Allah ba abinda bazai amfane ku komai ba, bazai cuce kuda komai ba (idan baku bauta masaba). Tur;daku ,da abinda kuke bautawa ba Allah ba. Shin bakuda hankali ne (ku gane wađannan gumaka basu cancanci bauta ba Allah ne. kadai ya cancanci bauta?)"
67. Sukace, "Ku ƙone shi (Ibrahima) ku taimaki iyayen gijinku (da ƙ one shi in kun kasance masu taimakon iyayen gijinku)". (Suka tara kirigar Itace, suka cinna wuta a cikin dukkansa, suka tamke Annabi Ibrahimu suka sanyashi cikin majajjawa sukajefa cikin wuta.)
68. Mukace "Yake wuta ki zamo sanyi da lafiya sumul a bisa Annabi Ibrahim" (bata ƙona komai daga gareshi ba sai đaurеđauren sa, zafinta ya kau, haskenta ya wanzu saboda fađinsa (Wasalaman) Yakuɓuta daga mutuwa ta sanyin da yake cikin wuta.)
69. Suka nufi kaidi dashi (shine ƙonewa,) muka sanya su taɓaɓɓu (cikin muradinsu.)
70. Muka tserar dashi da Annabi Luđu (đan đan'uwansa Haranu daga Irak) izuwa ƙasa wacce mukayi albarka cikinta ga talikai (da yawan ƙoramu da itatuwa [1] Itace Sham. Annabi Ibrahimu ya sauka Falasđinu, Annabi luđu ya sauka a Muntafiƙatu tafiyar wunice tsakaninsu.)
71. Muka baiwa Annabi Ibrahim Ishaka (alaihimussalamu, bayan ya roƙi đa,) muka bashi Annabi Yaƙubu ƙari (a kan abinda ya roƙa shine đanđa,) kowane (dagashi Annabi Ibrahimu da 'ya'yansa guda biyu) mun sanya su salihai (Annabawa.)

1) Hakana da yawan Annabawa da waliyyai da salihai - Sanajiy -

وَجَعَلْنَٰهُمْ أَيِمَّةً يَهْدُونَ بِأَمْرِنَا وَأَوْحَيْنَآ إِلَيْهِمْ فِعْلَ
ٱلْخَيْرَٰتِ وَإِقَامَ ٱلصَّلَوٰةِ وَإِيتَآءَ ٱلزَّكَوٰةِ ۖ وَكَانُواْ لَنَا
عَٰبِدِينَ ۖ ﴿٧٢﴾ * وَلُوطًا ءَاتَيْنَٰهُ حُكْمًا وَعِلْمًا وَنَجَّيْنَٰهُ مِنَ ٱلْقَرْيَةِ ثمن
ٱلَّتِي كَانَت تَّعْمَلُ ٱلْخَبَٰٓئِثَ ۖ إِنَّهُمْ كَانُواْ قَوْمَ سَوْءٍ فَٰسِقِينَ ۖ ﴿٧٣﴾
وَأَدْخَلْنَٰهُ فِي رَحْمَتِنَآ ۖ إِنَّهُۥ مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ۖ ﴿٧٤﴾ وَنُوحًا
إِذْ نَادَىٰ مِن قَبْلُ فَاسْتَجَبْنَا لَهُۥ فَنَجَّيْنَٰهُ وَأَهْلَهُۥ مِنَ ٱلْكَرْبِ
ٱلْعَظِيمِ ۖ ﴿٧٥﴾ وَنَصَرْنَٰهُ مِنَ ٱلْقَوْمِ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَآ ۖ
إِنَّهُمْ كَانُواْ قَوْمَ سَوْءٍ فَأَغْرَقْنَٰهُمْ أَجْمَعِينَ ۖ ﴿٧٦﴾ وَدَاوُۥدَ
وَسُلَيْمَٰنَ إِذْ يَحْكُمَٰنِ فِي ٱلْحَرْثِ إِذْ نَفَشَتْ فِيهِ
غَنَمُ ٱلْقَوْمِ ۖ وَكُنَّا لِحُكْمِهِمْ شَٰهِدِينَ ۖ ﴿٧٧﴾ فَفَهَّمْنَٰهَا
سُلَيْمَٰنَ ۖ وَكُلًّا ءَاتَيْنَا حُكْمًا وَعِلْمًا ۖ وَسَخَّرْنَا مَعَ دَاوُۥدَ
ٱلْجِبَالَ يُسَبِّحْنَ وَٱلطَّيْرَ ۖ وَكُنَّا فَٰعِلِينَ ۖ ﴿٧٨﴾ وَعَلَّمْنَٰهُ صَنْعَةَ
لَبُوسٍ لَّكُمْ لِيُحْصِنَكُم مِّنۢ بَأْسِكُمْ ۖ فَهَلْ أَنتُمْ شَٰكِرُونَ ۖ ﴿٧٩﴾
وَلِسُلَيْمَٰنَ ٱلرِّيحَ عَاصِفَةً تَجْرِي بِأَمْرِهِۦٓ إِلَى ٱلْأَرْضِ
ٱلَّتِي بَٰرَكْنَا فِيهَا ۖ وَكُنَّا بِكُلِّ شَيْءٍ عَٰلِمِينَ ۖ ﴿٨٠﴾

72. Mun sanya su limamai dasuke shiriyar (mutane izuwa addininmu) da izninmu da umarninmu, munyi musu wahayin aikin alherai izuwa garesu da tsaida salla da bada zakka, sun kasance masu biyayya a garemu.

(WANI ABU NA DAGA ƘISSAR ANNABI LUƊU DA ANNABI NUHU ALAIHIMUSSALAMU)

73. Mun baiwa Annabi Luɗu (alaihissalamu) hukunci (wato gwanintar shari'a tsakanin makaraya) da ilimi, mun tserar dashi daga alƙarya wacce take aikata miyagun ayyuka, (neman maza da harbi da bindiga da wasa da tsintsaye da wanin wannan,) haƙiƙa su sun kasance miyagun mutane fasikai.
74. Mun shigar dashi cikin jinƙanmu (da muka tserar dashi daga mutanensa) haƙiƙa shi Annabi Luɗu yana daga cikin cikakkun mutanen kirki.
75. Ambaci Annabi Nuhu (alaihissalamu) zamanin dayayi mummunar a addu'a a kan mutanensa dayace Ubangiji (kadaka bar hau izuma ƙarshenta) tun gaban (Annabi Ibrahim da Annabi Luɗu,) muka amsa masa, muka tserar dashi da iyalinsa (waɗanda suke tare dashi a cikin jirginsa) daga baƙin ciki maigirma, (shine nitsewa da ƙaryatawan mutanensa gareshi.)
76. Muka taimake shi a kan mutanen nan da suka ƙaryata da ayoyinmu (masu shiryarwa izuwa kan aikensa don kadasu sameshi da mummuna.) Haƙiƙa su sun kasance mutanen banza sai muka nutsar dasu baki ɗaya.

(WANI ABU NADAGA ƘISSAR ANNABI DAWUDU DASULAIMAN ALAIHIMUSSALAMU)

77. Ambaci labarin Annabi Dawuda da sulaiman (alaihimussalamu, zamanin da suka hukunci a cikin hatsin (wata gona) zamanin da dabbobin mutane sukayi kiwo cikin dare bada makiyayi ba (shine suka tsinke) mun kasance mahalarta ga hukuncinsu (Annabi Dawuda yace mai gona a bashi dabbobi da sukayi ta'adi a gonarsa, Annabi Sulaiman yace yayi amfani da cin gajiyar nomanta da "ya'yan da gasunta har izuwa hatsi yakoma irin yadda yake da kulawar maigona kuma a mayar da tumakai izuwa masu su.)
78. Muka fahintar da Annabi Sulaiman haƙiƙanin wannan shari'a, kowane daga cikinsu Munbashi gwanintar shari'a da Annabci da sani na al'amuran addini, muka hore duwarwatsu tareda Annabi Dawuda suna tasbihi tare dashi, hakana tsuntsaye, mun tabbata masu aikata wannan horewa (ko da yake abin mana ki ne gurin ku.)
79. Mun sanar dashi ƙera sulke, (shine farkon wanda ya aikatata, daga gabansa fate -fate ake yi) an koya masa wannan aiki saboda amfaninku donta katangance ku daga tsananin yaƙi ku (tareda magautanku,) To, shin! ku zaku gode wa Ubangiji wannan ni'ima.
80. Mun hore iska ga Annabi Sulaiman, tana gudu da umarninsa izuwa ƙasa wacce mukayi albarka a cikinta (Itace Sham,) mun kasance masanane ga kowane abu, (yana daga wancananka cewa yasan abinda ya baiwa Annabi Sulaiman zai komo dashi izuwa ƙanƙanda- kai ga Allah.)

وَمِنَ ٱلشَّيَٰطِينِ مَن يَغُوصُونَ لَهُۥ وَيَعْمَلُونَ عَمَلًا
دُونَ ذَٰلِكَ وَكُنَّا لَهُمْ حَٰفِظِينَ ﴿٨٢﴾ وَأَيُّوبَ إِذْ نَادَىٰ رَبَّهُۥٓ
أَنِّى مَسَّنِىَ ٱلضُّرُّ وَأَنتَ أَرْحَمُ ٱلرَّٰحِمِينَ ﴿٨٣﴾ فَٱسْتَجَبْنَا لَهُۥ
فَكَشَفْنَا مَا بِهِۦ مِن ضُرٍّ وَءَاتَيْنَٰهُ أَهْلَهُۥ وَمِثْلَهُم
مَّعَهُمْ رَحْمَةً مِّنْ عِندِنَا وَذِكْرَىٰ لِلْعَٰبِدِينَ ﴿٨٤﴾
وَإِسْمَٰعِيلَ وَإِدْرِيسَ وَذَا ٱلْكِفْلِ كُلٌّ مِّنَ
ٱلصَّٰبِرِينَ ﴿٨٥﴾ وَأَدْخَلْنَٰهُمْ فِى رَحْمَتِنَآ إِنَّهُم مِّنَ
ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿٨٦﴾ ۞ وَذَا ٱلنُّونِ إِذ ذَّهَبَ مُغَٰضِبًا فَظَنَّ
أَن لَّن نَّقْدِرَ عَلَيْهِ فَنَادَىٰ فِى ٱلظُّلُمَٰتِ أَن لَّآ إِلَٰهَ
إِلَّآ أَنتَ سُبْحَٰنَكَ إِنِّى كُنتُ مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٨٧﴾
فَٱسْتَجَبْنَا لَهُۥ وَنَجَّيْنَٰهُ مِنَ ٱلْغَمِّ وَكَذَٰلِكَ
نُۨجِى ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٨٨﴾ وَزَكَرِيَّآ إِذْ نَادَىٰ رَبَّهُۥ
رَبِّ لَا تَذَرْنِى فَرْدًا وَأَنتَ خَيْرُ ٱلْوَٰرِثِينَ ﴿٨٩﴾ فَٱسْتَجَبْنَا لَهُۥ
وَوَهَبْنَا لَهُۥ يَحْيَىٰ وَأَصْلَحْنَا لَهُۥ زَوْجَهُۥٓ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ يُسَٰرِعُونَ
فِى ٱلْخَيْرَٰتِ وَيَدْعُونَنَا رَغَبًا وَرَهَبًا وَكَانُوا۟ لَنَا خَٰشِعِينَ ﴿٩٠﴾

ربع

81. Akwai daga shaiɗanu waɗanda muka hore masa su suke nutso (a cikin kogi su fito da lu'u-lu'u da murjanai ga Annabi Sulaiman alaihissalam) suna aikata aiki komabayan wannan (nutson na ginegine da waninsu,) mun kasance masu kiyayewa garesu (dagasu ɓata abinda suka aikata (saboda sun kasance idan sun gama cikin dare saisu ɓatashi idan ba a basu wani ba.)

(ƘISSAR ANNABI AYYUBA ALAIHISSALAM)

82. Ambaci Annabi Ayyuba (alaihissalam) yayin da yake roƙon ubangijinsa, (lokacin da aka jarrabe shi da rasa dukkanin dukiyarsa da "ya"yansa da kyarkecewar jikinsa da ƙauracewar mutane gareshi, sai mata tasa kaɗai shekara uku ko bakwai da ƙuncin abincinsa.) Haƙiƙa ni tsanani ya same ni, kaine mafi jinƙan masu jinƙai.

83. Muka amsa roƙonsa, muka yaye masa abinda yake tare dashi na daga tsanani, muka bashi iyalinsa ('ya'yansa mazaje da mataye, aka raya kowanne daga nau'in nan guda biyu su uku ko bakwai misalinsu tare dasu na daga mastara - akayi ƙari cikin ƙuruciyarta yana da mashanyi na alkama da mashanyi na sha'ir, sai Allah ya aiko da girgije guda biyu ta tsuga ruwan zinariya a mashanyin alkama, ta tsuga ruwan azurfa a mashanyin sha'ir har suka dinga kwarara) don jinƙai daga garemu da gargaɗi ga masu bauta ga Allah.

(WANI ABU DAGA ƘISSAR ISMAILA DA IDRIS DA ZULKIFLI ALAIHIMUSSALAMU)

84. Ambaci labarin Annabi Ismaila da Annabi Idrisa da Zulkifli (alaihimussalamu) kowane ɗaya daga garesu (yana cikin masu haƙuri a bisa ɗa'ar Allah da haƙuri ga buran saɓon Allah.)

85. Mun shigar dasu cikin rahamarmu (wato Annabci) haƙiƙa su suna daga cikin salihai, (an ambace shi Zulkifli[1] saboda ya lamunce azumin dukkan wuninsa da tsaiwar dukkan darensa, kuma zaiyi hukunci tsakanin mutane bada fushi ba, ya cika da wannan.

(ƘISSAR ANNABI YUNUSA ALAIHIS-SALAM, AKWAI AMBATON AMFANIN ADDU'A A CIKI)

86. Ambaci Zannunu ma'abucin kifi shine Yunusa ɗan Matta alaihissalam) zamanin daya tafi yana mai fushi (da mutanensa saboda yayi gwagwarmaya dasu ba ayi masa izni cikin wannan fitar ba,) ya zaci bazamu ƙuntata a gareshi ba, (da abinda muka hukunta a gareshi da tsare shi cikin kifi) sai yayi kira a cikin duffai (duhun dare, duhun kogi, duhun cikin kifi,) Cewa babu abin bautada gaskiya sai kai. Tsarki ya tabbatar maka, haƙiƙa ni na kasance daga cikin azzalumai (a cikin tafiyata tsakanin mutanena bada iznin ka ba.)

87. Muka amsa masa muka tserar dashi daga baƙin ciki (da wancananka kalmomi) tamfar da muka tserar dashi muke tserar da muminai (na daga baƙin cikinsu idan sun nemi taimako damu suna masu addu'a.)

(ƘISSAR ANNABI ZAKARIYA'U DA YAHAYA DA MARYAMU)

88. Ambaci Annabi Zakariya'u zamanin daya kira Ubangijinsa, (yace) "Ubangiji kadaka barni ni kaɗai (bada da dazai gajeni ba,) kaine fiyayyen magada (mai wanzuwa bayan halittarka.)

89. Muka amsa masa (roƙonsa) muka bashi Annabi Yahaya ɗansa, muka gyara masa matarsa tazoda ɗa tana bakarara haƙiƙa su sun kasance suna gaggawa a cikin aikin alhairai suna roƙonmu don kwaɗayi (cikin jinƙanmu) da tsoro (daga azabarmu). Kai, haƙiƙa sun kasance masu ƙanƙan-dakai a garemu.

وَالَّتِي أَحْصَنَتْ فَرْجَهَا فَنَفَخْنَا فِيهَا مِن رُّوحِنَا
وَجَعَلْنَاهَا وَابْنَهَا ءَايَةً لِّلْعَالَمِينَ ﴿90﴾ إِنَّ هَٰذِهِ
أُمَّتُكُمْ أُمَّةً وَاحِدَةً وَأَنَا رَبُّكُمْ فَاعْبُدُونِ ﴿91﴾
وَتَقَطَّعُوا أَمْرَهُم بَيْنَهُمْ كُلٌّ إِلَيْنَا رَاجِعُونَ ﴿92﴾
فَمَن يَعْمَلْ مِنَ الصَّالِحَاتِ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَلَا كُفْرَانَ
لِسَعْيِهِ وَإِنَّا لَهُ كَاتِبُونَ ﴿93﴾ وَحَرَامٌ عَلَىٰ قَرْيَةٍ
أَهْلَكْنَاهَا أَنَّهُمْ لَا يَرْجِعُونَ ﴿94﴾ حَتَّىٰ إِذَا فُتِحَتْ
يَاجُوجُ وَمَاجُوجُ وَهُم مِّن كُلِّ حَدَبٍ يَنسِلُونَ ﴿95﴾
وَاقْتَرَبَ الْوَعْدُ الْحَقُّ فَإِذَا هِيَ شَاخِصَةٌ
أَبْصَارُ الَّذِينَ كَفَرُوا يَا وَيْلَنَا قَدْ كُنَّا
فِي غَفْلَةٍ مِّنْ هَٰذَا بَلْ كُنَّا ظَالِمِينَ ﴿96﴾ إِنَّكُمْ
وَمَا تَعْبُدُونَ مِن دُونِ اللَّهِ حَصَبُ
جَهَنَّمَ أَنتُمْ لَهَا وَارِدُونَ ﴿97﴾ لَوْ كَانَ هَٰؤُلَاءِ ءَالِهَةً
مَّا وَرَدُوهَا وَكُلٌّ فِيهَا خَالِدُونَ ﴿98﴾
لَهُمْ فِيهَا زَفِيرٌ وَهُمْ فِيهَا لَا يَسْمَعُونَ ﴿99﴾

90. Ka ambaci Maryamu wacce ta kiyaye farjinta (daga a same shi,) sai mukayi busa a cikinta daga rai da muka halicce shi daga garemu (Jibrilu yayi busa a cikin aljihun rigarta saita samu cikin Annabi Isa alaihissalamu.) Mun sanyata da ɗanta aya ga talikai. (mutane da Mala'ikuda aljannu ta inda.ta haife shi bada miji ba.)

(WAHDATUL ISLAM) WATO DAYANTAKAR MUSULMI DA MUSULUNCI

91. Haƙiƙa wannan addini Musulunci shine addininku (Yaku Mahammadawa, ai wajibi ne ku kasance a kanta) al'umma guda ɗaya, kuma nine ubangijinku ku bauta min (tareda kaɗaita ni.)
92. Sai suka rarraba sha'anin addininsu a tsakaninsu (suka sassaɓa a cikinsa kungiyoyin Yahudu da Nasara, Ubangiji yace) "Kowanne mai komowa ne izuwa garemu".
93. Duka wanda yayi aiki daga ayyuka nagargaru alhali yana mumini to, ba butulcewa da aikinsa, haƙiƙa mu masu rubutawa ne gareshi, (zamu umarci Mala'iku su rubutamu yi sakamako.)
94. Haramun ne bisa alƙarya da muka halakar da mutanenta cewa su komo (duniya).

(YAJUJU DA MAJUJU)

95. Har lokacin da aka buɗe Yajuju da Majuju, (wato toshiyar da akayi musu, wancananka kuma zai auku kusa da tashin alƙiyama,) su suna gaggawa daga dukkan tudu.
96. Wa'adi na gaskiya Yakusanta (shine ranar Alƙiyama,) Kumfa sai gata (ai ƙissar) idandunan waɗanda suka kafirta sun bayyana tulu-tulu (saboda tsananin wancananka rana,) suna cewa "Wo-ho-ho, ya kaitonmu, haƙiƙa mun kasance (a duniya) a cikin rabkana daga wannan (rana), kai mun kasance azzalumai (ga kanmu saboda ƙaryatawar manzanni)".

(ƘARSHEN AL'AMARIN KAFIRAI DA ƘARSHEN MUMINAI)

97. Haƙiƙa ku (Ya mutanen makka da makamantansu) da abinda kuke bautawa ba Allah ba, guma-guman Jahannama ne ku, ku masu zundumawa ne a cikinta.
98. Da waɗannan gumaka iyayen giji ne (tamfar yadda kuka riya) da basu zunduma cikinta ba kowane daya daga masu bautada abin bautawa madawwama ne a cikinta.
99. kumruwa tana garesu (masu bautar nan) a cikinta, su suna cikinta basa jin (wani abu saboda tsananin ruguginta. Yayin da wannan aya ta sauka sai ɗan Zibi'ira yace an bautawa Uzairu da Masihu da Mala'iku, to, su ashe suna cikin wutar ke nan, sai Allah yace:)

ثمن

* إِنَّ ٱلَّذِينَ سَبَقَتْ لَهُم مِّنَّا ٱلْحُسْنَىٰٓ أُوْلَٰٓئِكَ عَنْهَا مُبْعَدُونَ ﴿100﴾
لَا يَسْمَعُونَ حَسِيسَهَا وَهُمْ فِي مَا ٱشْتَهَتْ أَنفُسُهُمْ خَٰلِدُونَ ﴿101﴾
لَا يُحْزِنُهُمُ ٱلْفَزَعُ ٱلْأَكْبَرُ وَتَتَلَقَّىٰهُمُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ
هَٰذَا يَوْمُكُمُ ٱلَّذِي كُنتُمْ تُوعَدُونَ ﴿102﴾ يَوْمَ نَطْوِي
ٱلسَّمَآءَ كَطَيِّ ٱلسِّجِلِّ لِلْكِتَٰبِ كَمَا بَدَأْنَا أَوَّلَ خَلْقٍ نُّعِيدُهُۥ
وَعْدًا عَلَيْنَآ إِنَّا كُنَّا فَٰعِلِينَ ﴿103﴾ وَلَقَدْ كَتَبْنَا
فِي ٱلزَّبُورِ مِنۢ بَعْدِ ٱلذِّكْرِ أَنَّ ٱلْأَرْضَ يَرِثُهَا
عِبَادِيَ ٱلصَّٰلِحُونَ ﴿104﴾ إِنَّ فِي هَٰذَا لَبَلَٰغًا لِّقَوْمٍ
عَٰبِدِينَ ﴿105﴾ وَمَآ أَرْسَلْنَٰكَ إِلَّا رَحْمَةً لِّلْعَٰلَمِينَ ﴿106﴾
قُلْ إِنَّمَا يُوحَىٰٓ إِلَيَّ أَنَّمَآ إِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَٰحِدٌ فَهَلْ أَنتُم
مُّسْلِمُونَ ﴿107﴾ فَإِن تَوَلَّوْاْ فَقُلْ ءَاذَنتُكُمْ عَلَىٰ سَوَآءٍ
وَإِنْ أَدْرِيٓ أَقَرِيبٌ أَم بَعِيدٌ مَّا تُوعَدُونَ ﴿108﴾ إِنَّهُۥ يَعْلَمُ ٱلْجَهْرَ
مِنَ ٱلْقَوْلِ وَيَعْلَمُ مَا تَكْتُمُونَ ﴿109﴾ وَإِنْ أَدْرِي لَعَلَّهُۥ
فِتْنَةٌ لَّكُمْ وَمَتَٰعٌ إِلَىٰ حِينٍ ﴿110﴾ قُل رَّبِّ ٱحْكُم
بِٱلْحَقِّ وَرَبُّنَا ٱلرَّحْمَٰنُ ٱلْمُسْتَعَانُ عَلَىٰ مَا تَصِفُونَ ﴿111﴾

100. Haƙiƙa waɗanda daraja mafi kyau ta rigaya a garesu daga garemu, waɗancananka ababan nisantawa ne ga buranta.
101. Baza suji amanta ba, su madawwama ne a cikin abinda ransu take marmari (na ni'ima.)
102. Razani mafi girma bazai baƙanta musu ba, (shine ayi umarni da bawa izuwa wuta,) Mala'iku zata tarye su (yayin fitowarsu daga kaburburansu suna cewa dasu) "Wannan shine ranarku wanda aka kasance anayi muku alƙawari (da ita a duniya.)
103. Ambaci ranar da muke naɗe sama kamar naɗewar takarda [1] ga abin rubutawa, tamfar yadda muka tara farkon halitta (daga rashi) muke maidashi (bayan rasuwarsa,) wannan alƙawari ne a kanmu, mu haƙiƙa mun kasance masu aikata (abinda muka alƙawarta.)
104. Haƙiƙa mun rubuta a cikin littattafan da Allah ya saukar bayan Uwar littafi wanda yake gurin Allah, haƙiƙa ƙasar aljanna bayina managarta [2] ne suke gadonta.
105. Haƙiƙa a cikin wannan alƙur'ani akwai iyarwa a cikin shiga aljanna ga mutane masu aiki dashi.

(SANIN MATSAYIN ANNABI SALALLAHU ALAIHI WASALLAMA DAGA MUTANE)

106. Bamu aikoka (Ya Muhammadu Sallallahu alaika wasallama) sai don jinƙan halitta mutum da aljan.
107. Cene, " Haƙiƙa ni ana aikowa ne izuwa gareni, cewa Ubangijinku Allah ne maɗayancin Sarki kawai. Shin ba kwa jawu ba (izuwa abinda aka aiko nadaga ɗayantar Allah.)
108. To, in sun bada baya (ga buran wannan,) to cene (dasu) "Na sanar daku ,da (yaƙi,) muna madaidaita daku ,a cikin saninsa, bani kaɗai na sani ba,) Ni ban san abinda ake muku narko dashi (na azaba manesanci ne) ko makusanci ne ba.
109. Haƙiƙa Ubangiji Maɗaukakin Sarki ne yasan abinda aka bayyana (na magana da aiki, naku ko na waninku,) yasan abinda kuke ɓoyewa (kuda waninku nadaga asiri.)
110. Ni ban saniba wata kila abinda na sanashsheku shi ɗin nan ba a san lokacinsa fitina ne gareku (don a ga abinda zaku aikata) da ɗan shaƙata muku izuwa ƙarewar ajalinku.
111. Cene, "Ya Ubangijina, yi hukunci da gaskiya (tsakanina da masu ƙaryata ni shine kayi musu azaba koka taimake mu a kansu, akayi musu azabar kuwa a ranar Badar da Uhudu da Ahzabu, da Hunainu, da Handaku aka taimake shi a kansu.) Ubangijinmu mai yawan jinƙai ne abin neman taimako a bisa abinda kuke sufantawa (nadaga ƙaryarku bisa Ubangiji a cikin faɗinku ya riƙi ɗa da ƙaryarku gareni a cikin faɗinku ni matsafi ne da ƙaryarku ga alƙur'ani a cikin faɗinku waƙa ne.)

1) daukar sijjilu a kan sunan cewa mala'ikane, akwai nisa dan gane da bayyanar ma'ana, saboda mu bazamu iya fahimtar yadda mala'ika yake nade takarda ba don ba abin ganin mu bane. - Sanajy - 2) Abin nufi da salihi anan wato ana nufin dukkan salihi na wannan Al'umma da waninta, wato wanda ya cika da imani (sawii)

22 سُورَةُ الحَجِّ مَدَنِيَّة
وَهِيَ سِتٌّ وَسَبْعُونَ ءَايَةً 76

حزب

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

يَا أَيُّهَا النَّاسُ اتَّقُوا رَبَّكُمْ إِنَّ زَلْزَلَةَ السَّاعَةِ شَيْءٌ عَظِيمٌ ﴿1﴾
يَوْمَ تَرَوْنَهَا تَذْهَلُ كُلُّ مُرْضِعَةٍ عَمَّا أَرْضَعَتْ وَتَضَعُ
كُلُّ ذَاتِ حَمْلٍ حَمْلَهَا وَتَرَى النَّاسَ سُكَارَىٰ وَمَا هُم بِسُكَارَىٰ
وَلَٰكِنَّ عَذَابَ اللَّهِ شَدِيدٌ ﴿2﴾ وَمِنَ النَّاسِ مَن يُجَادِلُ فِي اللَّهِ بِغَيْرِ عِلْمٍ
وَيَتَّبِعُ كُلَّ شَيْطَانٍ مَّرِيدٍ ﴿3﴾ كُتِبَ عَلَيْهِ أَنَّهُ مَن تَوَلَّاهُ
فَأَنَّهُ يُضِلُّهُ وَيَهْدِيهِ إِلَىٰ عَذَابِ السَّعِيرِ ﴿4﴾ يَا أَيُّهَا النَّاسُ إِن كُنتُمْ
فِي رَيْبٍ مِّنَ الْبَعْثِ فَإِنَّا خَلَقْنَاكُم مِّن تُرَابٍ ثُمَّ مِن نُّطْفَةٍ
ثُمَّ مِنْ عَلَقَةٍ ثُمَّ مِن مُّضْغَةٍ مُّخَلَّقَةٍ وَغَيْرِ مُخَلَّقَةٍ لِّنُبَيِّنَ لَكُمْ
وَنُقِرُّ فِي الْأَرْحَامِ مَا نَشَاءُ إِلَىٰ أَجَلٍ مُّسَمًّى ثُمَّ نُخْرِجُكُمْ طِفْلًا
ثُمَّ لِتَبْلُغُوا أَشُدَّكُمْ وَمِنكُم مَّن يُتَوَفَّىٰ وَمِنكُم مَّن يُرَدُّ إِلَىٰ أَرْذَلِ الْعُمُرِ
لِكَيْلَا يَعْلَمَ مِن بَعْدِ عِلْمٍ شَيْئًا وَتَرَى الْأَرْضَ هَامِدَةً
فَإِذَا أَنزَلْنَا عَلَيْهَا الْمَاءَ اهْتَزَّتْ وَرَبَتْ وَأَنبَتَتْ مِن كُلِّ زَوْجٍ بَهِيجٍ ﴿5﴾

Suratul Hajji

A Madina Aka. Saukar Da Ita Ayoyinta Saba'in. Dashida (76)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

"Ita wannan sura ta ƙunshi magana a kan tashin alƙiyama da ba'alin matsayantada magana kan mushirikai da matsayinsu a kan masallaci mai alfarma da kuma magana a kan dakin Ka'abada aikace"aikacen Hajji, da zance kan masu ƙaryatawa da bugar dasu don wa'azantuwa dasu. A karshen surar kuma akwai nuna girman Ubangiji a cikin kasan-tattu tareda sanya misali ga iyayen giji"

(KIRA IZUWA TSORON ALLAH DA TASHIN ALƘIYAMA)

1. Yaku mutane, kuji tsoron Ubangijinku (shine kubishi,) haƙiƙa girgizar sa'a zata kasance bayan hudowar rana daga yamma,) abune maigirma (a cikin firgita mutane, wandashi kansa nau'i ne na azaba.)
2. Ranar dakake ganin girgizan nan dukkan mai shada nono tana rabkana ga buran abinda take shayarwa, dukkan mai ciki tana haife cikinta, kana ganin mutane masu maye (saboda tsananin tsoro,) alhalisu ba masu mayene (saboda shan giya) ba, saidai azabar Ubangijice matsananciya. (Wannan ayata sauka a cikin Nalaru ɗan harisu da waɗansu jama'a.)
3. Akwai daga mutane wanda yake jayayya da Allah bada ilimiba, (sukece wa Mala'iku 'ya'yayen Allahne, Alƙur'ani surace suracen mutan farkone, sukayi musun tashin alƙiyama da raya wanda ya zama turɓaya,) yake bin dukkan shaiɗani mai taurin kai (a cikin jayayyarsa.)
4. An wajabta a kan shaiɗanin nan cewa wanda ya jiɓinceshi, haƙiƙa shi zai ɓatar dashi, zaikirashi izuwa azabar wuta.

(WANI ABU DAGA DALILAN TASHIN ALƘIYAMA)

5. Yaku mutane in kun kasance cikin kokonto daga tashin alƙiyama haƙiƙa mu mun halicceku (wato asalinku Annabi Adamu) daga turbaya sannan (muka halicci zurriyarsa) daga nuɗufa, maniyyi, sannan daga gudan jini, sannan daga tsoka, cikakkiyar halitta da watan cikakkiyar halitta donmu bayyana muku (cikar ikonmu donku kafa dalili da ƙudurarmu a cikin fara halitta a kan maida ita.) Muna tabbatar da abinda muka ga dama a cikin mahaifa izuwa ajali abin ambato (lokacin fitowarsa, sannan muna fitardaku ,daga cukkunan iyayenku mata kuna jarirai) sannan mu rayaku, dominku isa cikar ƙarfinku, (shine daga shekara talatin izuwa arba'in ,) akwai daga cikinku wanda ake karɓar ransa tun baikai cikar ƙarfinsa ba, akwai daga gareku wanda ake maidashi izuwa wulaƙantaccen rai, (tsufa) tukuf-tukuf don kada yasan komai bayan sani, (Ikrimatu yace, Wanda ya karanta Alƙur'ani bazai zama cikin wannan hali ba, amma malamai su hankalinsu yana ƙaruwa ne koda yaushe ransu ya tsawaita kamar yadda yake abin gani-Sawii). Kana ganin ƙasa tana ƙeƙasashshiya idan mun saukar da ruwa kanta saitakan motsata tofu tsirar daga dukkan nau'o'i kyawawa, (wannan abin ambato na fara halittar mutum izuwa ƙarshen raya ƙasa-).

ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْحَقُّ وَأَنَّهُۥ يُحْىِ ٱلْمَوْتَىٰ وَأَنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ
قَدِيرٌ ﴿6﴾ وَأَنَّ ٱلسَّاعَةَ ءَاتِيَةٌ لَّا رَيْبَ فِيهَا وَأَنَّ ٱللَّهَ يَبْعَثُ مَن
فِى ٱلْقُبُورِ ﴿7﴾ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يُجَٰدِلُ فِى ٱللَّهِ بِغَيْرِ عِلْمٍ وَلَا هُدًى
وَلَا كِتَٰبٍ مُّنِيرٍ ﴿8﴾ ثَانِىَ عِطْفِهِۦ لِيُضِلَّ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ لَهُۥ فِى ٱلدُّنْيَا
خِزْىٌ وَنُذِيقُهُۥ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ عَذَابَ ٱلْحَرِيقِ ﴿9﴾ ذَٰلِكَ بِمَا قَدَّمَتْ
يَدَاكَ وَأَنَّ ٱللَّهَ لَيْسَ بِظَلَّٰمٍ لِّلْعَبِيدِ ﴿10﴾ * وَمِنَ ٱلنَّاسِ ثمن
مَن يَعْبُدُ ٱللَّهَ عَلَىٰ حَرْفٍ فَإِنْ أَصَابَهُۥ خَيْرٌ ٱطْمَأَنَّ بِهِۦ
وَإِنْ أَصَابَتْهُ فِتْنَةٌ ٱنقَلَبَ عَلَىٰ وَجْهِهِۦ خَسِرَ ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةَ
ذَٰلِكَ هُوَ ٱلْخُسْرَانُ ٱلْمُبِينُ ﴿11﴾ يَدْعُوا۟ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَضُرُّهُۥ
وَمَا لَا يَنفَعُهُۥ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلضَّلَٰلُ ٱلْبَعِيدُ ﴿12﴾ يَدْعُوا۟ لَمَن ضَرُّهُۥٓ أَقْرَبُ
مِن نَّفْعِهِۦ لَبِئْسَ ٱلْمَوْلَىٰ وَلَبِئْسَ ٱلْعَشِيرُ ﴿13﴾ إِنَّ ٱللَّهَ يُدْخِلُ
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا
ٱلْأَنْهَٰرُ إِنَّ ٱللَّهَ يَفْعَلُ مَا يُرِيدُ ﴿14﴾ مَن كَانَ يَظُنُّ
أَن لَّن يَنصُرَهُ ٱللَّهُ فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ فَلْيَمْدُدْ بِسَبَبٍ إِلَى ٱلسَّمَآءِ
ثُمَّ لْيَقْطَعْ فَلْيَنظُرْ هَلْ يُذْهِبَنَّ كَيْدُهُۥ مَا يَغِيظُ ﴿15﴾

6. Saboda cewa haƙiƙa Allah shine kadai matabbacin dauwama kuma shine mai raya matattu kuma shi mai ikone bisa komai.
7. Kuma haƙiƙa alƙiyama mai zuwace ba kokwanto a cikinta, kuma haƙiƙa Ubangiji yana tashin waɗanda suke cikin ƙaburbura.

(MUTANE IRI IRINE)

8. Akwai daga mutane wanda yake jayayya da Allah bada ilimi ba bada shiriya da take taredashi ba, (ta sauka ne a cikin AbuJahil) fir aunan wannan ALumma bada littafi mai haske ba.
9. Yana mai fusfusge wuyansa (don girman kai ga buran imani dama ko hagun,) donya ɓatar ga buran hanyar Allah. Kunyata ta tabbata gareshi a duniya, (an kashe shi ranar Badar,) zamu ɗanɗana masa azabar gobara. Jahannama aranar lahira.
10. (Anace masa) "Wancananka saboda abinda hannunka ta gabatar ne, kuma haƙiƙa Ubangiji barnai zalunci bane ga bayinsa (yayi musu azaba bada zunubi ba.)"
11. Akwai daga mutane wanda yake bautawa Allah a bisa gefe, (wato kokwanto a cikin ibadarsa,) idan alheri ya sameshi (lafiya a cikin kansa da dukiyarsa) saiya nutsu dashi, idan fitina ta sameshi (rashin lafiya a cikin kansa da dukiyarsa da sauran irinsu) saiya juya a kan fuskarsa (izuwa kafirci) ya tabe duniya (da tserewar burinsa) da lahira (saboda kafirci.) Wancananka shine haƙiƙan tabewa mabayyani.
12. Yana bautawa ba Allah ba (nadaga gunki) abinda bazai cuceshi ba (idan bai bauta masa ba,) bazai amfaneshi ba (inya bautar masa) wancananka (bautarnan) shine ainihin ɓata manisanci (ga buran gaskiya.)
13. Yana bautawa wanda cutarsa (inan bauta masa) tafi kusa da amfaninsa (in zaiyi amfanin takadiran,) tir! Mataimaki (shi,) tir! aboki (shi). (Ya biyanta ambaton mai konkwanto da taɓewa da ambaton muminai da sakamako a cikin faɗin)
14. Haƙiƙa Ubangiji yana shigar da waɗanda suka bada gaskiya sukayi ayyuka nagargaru (sune farilloli da nafilfilu, yana sanyasu) cikin aljannatai wacce ƙoramu take gudana ƙarƙashinta. Haƙiƙa Ubangiji yana aikata abinda yaga dama (na girmama wanda yabishi, da wulaƙanta wanda ya saɓeshi.)

(ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA DAN LELENBAWANE AWAJAN MAHALILCCI DA BAN KASHI GA "YAN WAHABIYYAWA DA IRINSU - RINSU)

15. Wanda ya kasance yana zato cewa Allah bazai taimaki Annabi Muhammadu ba (Sallallahu alaihi wasallama) a duniya da lahira (yamutu don fushi, shine) ya miƙa igiya izuwa sama (wato ai rufin ɗakinsa ya ɗaure igiyan nan da jikinsa da wuyansa, sannan ya yanke igiyar nan donya maƙure kansa da ita, to yaduba, yalla kaidinsa (a cikinsa a cikin kin taimakon Annabi Sallallahu alaihi wasallama) ya tafida abinda ya baƙanta masa? (wato ya maƙure ƙansa da kansa ba makawa daga taimakon Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama.)

وَكَذَٰلِكَ أَنزَلۡنَٰهُ ءَايَٰتِۭ بَيِّنَٰتٖ وَأَنَّ ٱللَّهَ يَهۡدِي مَن يُرِيدُ ﴿16﴾
إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَٱلَّذِينَ هَادُواْ وَٱلصَّٰبِـِٔينَ وَٱلنَّصَٰرَىٰ
وَٱلۡمَجُوسَ وَٱلَّذِينَ أَشۡرَكُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ يَفۡصِلُ بَيۡنَهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۚ
إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ شَهِيدٌ ﴿17﴾ أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ يَسۡجُدُۤ لَهُۥ مَن
فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِ وَٱلشَّمۡسُ وَٱلۡقَمَرُ وَٱلنُّجُومُ
وَٱلۡجِبَالُ وَٱلشَّجَرُ وَٱلدَّوَآبُّ وَكَثِيرٞ مِّنَ ٱلنَّاسِۖ
وَكَثِيرٌ حَقَّ عَلَيۡهِ ٱلۡعَذَابُۗ وَمَن يُهِنِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن مُّكۡرِمٍۚ
إِنَّ ٱللَّهَ يَفۡعَلُ مَا يَشَآءُ۩ ﴿18﴾ ۞هَٰذَانِ خَصۡمَانِ ٱخۡتَصَمُواْ فِي رَبِّهِمۡۖ
فَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ قُطِّعَتۡ لَهُمۡ ثِيَابٞ مِّن نَّارٖ يُصَبُّ
مِن فَوۡقِ رُءُوسِهِمُ ٱلۡحَمِيمُ يُصۡهَرُ بِهِۦ مَا فِي بُطُونِهِمۡ وَٱلۡجُلُودُ
وَلَهُم مَّقَٰمِعُ مِنۡ حَدِيدٖ ﴿19﴾ كُلَّمَآ أَرَادُوٓاْ أَن
يَخۡرُجُواْ مِنۡهَا مِنۡ غَمٍّ أُعِيدُواْ فِيهَا وَذُوقُواْ عَذَابَ ٱلۡحَرِيقِ ﴿20﴾
إِنَّ ٱللَّهَ يُدۡخِلُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ جَنَّٰتٖ
تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ يُحَلَّوۡنَ فِيهَا مِنۡ أَسَاوِرَ
مِن ذَهَبٖ وَلُؤۡلُؤٗاۖ وَلِبَاسُهُمۡ فِيهَا حَرِيرٞ ﴿21﴾

سجدة ربع

16. Misalin yadda muka saukar da ayoyin da suka rigaya, hakanan muka saukar da alƙur'ani mai wanzuwa, ayoyi mabayyana, haƙiƙa Ubangiji yana shiriyar wanda yaga damar (shiriyar dashi, Allah ka shiryemu ka kuma shiryi wanda dukkasan zai shiryu, Amin.)

(ADALCIN UBANGIJI DA ƘUDIRA TASA)

17. Haƙiƙa waɗanda suka bada gaskiya da yahudawa da Sabawa da Nasara da Maguzawa da waɗanda sukayi shirka da Allah, haƙiƙa Ubangiji yana rabewar hukunci tsakaninsu ranar alƙiyama, (ya shigar da muminai aljanna ya shigar da kafirai wuta,) haƙiƙa Ubangiji masanine da komai (sani na ƙarara.)

18. Shin baka sani ba haƙiƙa Ubangiji duk wanda ke cikin sama da wanda ke cikin ƙasa, da rana da wata, da taurari da duwarwatsu da itatuwa da dabbobi suna sajada ga Ubangiji bane da kuma yawaici daga mutane? Yawaici kuma azabace ta wajaba garesu (sune kafirai saboda sunƙi yin sajada).Duk wanda Allah ya wulaƙantashi (shine ya zama shaƙyi) to, ba mai girmama wa gareshi. Haƙiƙa Ubangiji yana aikata abinda yaga dama (na daga girmamawa da wulaƙantawa.

(KAFIRAI DA MUMINAI DA SAKAMAKON KOWANNE)

19. Waɗannan makarayane guda biyu sukayi husuma a cikin sha'anin (addinin) Ubangijinsu, to, waɗanda suka kafirta za a yanyanko musu tufafi na wuta (da zasu ɗaura su,) za a kwararo ruwan zafi a burbushin kawukansu, za a narke abinda yake cikin cukkunansu dashi (na daga kitsutsuwa da waninsu, ana soya fatunsu, (dashi.) Gudumar baƙin ƙarfe yana garesu, saboda dukan kawukansu.

20. Koda yaushe suka nufi fita daga wuta (saboda baƙin ciki dazai riskesu a cikinta,) sai a fafaresu a cikinta (a koma dasu da guduman nan izuwa gareta, a ce dasu;) "ku ɗanɗani kuɗar azabarku".

21. Haƙiƙa Ubangiji yana shigar da waɗanda sukayi ayyuka nagargaru aljannatai da ƙoramu suke kwarara daga ƙarƙashinsu anayi musu ƙawa a cikinta daga kwandagai na zinariya da lu'ulu'u abinɗaurawarsu a cikinta alharinine (wanda aka haramta ɗaura shi ga mazaje a duniya.)

(YAN DARIKA DA AIKIN SU)

وَهُدُوٓاْ إِلَى ٱلطَّيِّبِ مِنَ ٱلْقَوْلِ وَهُدُوٓاْ إِلَىٰ صِرَٰطِ ٱلْحَمِيدِ ﴿22﴾
إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَيَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ
ٱلَّذِے جَعَلْنَٰهُ لِلنَّاسِ سَوَآءٌ ٱلْعَٰكِفُ فِيهِ وَٱلْبَادِ
وَمَنْ يُرِدْ فِيهِ بِإِلْحَادِۭ بِظُلْمٍ نُذِقْهُ مِنْ عَذَابٍ
أَلِيمٍ ﴿23﴾ وَإِذْ بَوَّأْنَا لِإِبْرَٰهِيمَ مَكَانَ ٱلْبَيْتِ أَن لَّا تُشْرِكْ
بِے شَيْـًٔا وَطَهِّرْ بَيْتِيَ لِلطَّآئِفِينَ وَٱلْقَآئِمِينَ وَٱلرُّكَّعِ
ٱلسُّجُودِ ﴿24﴾ وَأَذِّن فِے ٱلنَّاسِ بِٱلْحَجِّ يَأْتُوكَ رِجَالًا
وَعَلَىٰ كُلِّ ضَامِرٍ يَأْتِينَ مِن كُلِّ فَجٍّ عَمِيقٍ ﴿25﴾
لِيَشْهَدُواْ مَنَٰفِعَ لَهُمْ وَيَذْكُرُواْ ٱسْمَ ٱللَّهِ فِے أَيَّامٍ
مَّعْلُومَٰتٍ عَلَىٰ مَا رَزَقَهُم مِّنۢ بَهِيمَةِ ٱلْأَنْعَٰمِ
فَكُلُواْ مِنْهَا وَأَطْعِمُواْ ٱلْبَآئِسَ ٱلْفَقِيرَ ﴿26﴾ ثُمَّ لِيَقْضُواْ
تَفَثَهُمْ وَلْيُوفُواْ نُذُورَهُمْ وَلْيَطَّوَّفُواْ بِٱلْبَيْتِ
ٱلْعَتِيقِ ﴿27﴾ * ذَٰلِكَ وَمَن يُعَظِّمْ حُرُمَٰتِ ٱللَّهِ فَهُوَ خَيْرٌ ثمن
لَّهُۥ عِندَ رَبِّهِۦ وَأُحِلَّتْ لَكُمُ ٱلْأَنْعَٰمُ إِلَّا مَا يُتْلَىٰ عَلَيْكُمْ
فَٱجْتَنِبُواْ ٱلرِّجْسَ مِنَ ٱلْأَوْثَٰنِ وَٱجْتَنِبُواْ قَوْلَ ٱلزُّورِ ﴿28﴾

22. An shiryesu a duniya izuwa daddaɗa na magana (shine La'ilaha Illallahu,) an shiryesu izuwa tafarki abin godewa (addinin Allah.)

HARAMCIN MASALLACI MAI ALFARMA, GA KAFIRAI DA SHIRYAR DA ANNABI IBRAHIMU MAHALLIN KA'ABA YAYIN DAZAI GINATA

23. Haƙiƙa waɗannan da suka kafirta suke hanawa ga buran addinin Allah, suke hanawa ga masallaci mai alfarma wanda muka sanyashi mabauta ga mutane, wanda da mazauni cikinsa da baƙo duk daidaine a cikinsa. Zamu ɗandɗana masa azaba mai raɗaɗi (kuma duka wanda yanufi kangara a cikinsa saboda zalunci shine ya aikata abin hani ko koda zagin hadimin, zamu ɗanɗana masa daga azaba mai raɗaɗi.)
24. Ka ambata zamanin da muka bayyana ga Annabi Ibrahim (alaihissalamu) gurin ɗaƙi (donya ginashi, ya kasance an ɗaukeshi zamanin Dufanu [1] muka umarceshi kada ka shirkanta komai tareda ni, kuma ka tsarkake ɗakina (daga gumaka,) don masu Dawafi da mazauna a cikinsa, da masu ruku'u masu sujada.

(HAJJIN DAKIN ALLAH MAI ALFARMA)

25. Kayi kira izuwa mutane da hajji (sai yayi kira a kan dutsen Abiƙubaisu, Yaku waɗannan mutane haƙiƙa Ubangiji ya gina ɗaki, ya wajabta hajjantarsa a gareku, to, ku amsawa Ubangijinku, ya juyo dama da fuskarsa hakana hagu da dama dayamma, duka wanda Allah yanufi zaiyi hajji ya amsa masa daga tsatson mazaje da mahaifa mataye, Labbaik- Allahumma-labbaika.) Sazo maka suna tafe a kan sawayensu, sazo maka suna haye a kan dukkan madankwari (raƙumi ramamme) su maɗankwaran sazo daga kowane loko mai nisa.
26. Donsu halarci amfanunuwansu (a duniya da lahira) su ambaci sunan Allah a cikin kwanuka ababan sani (goma na Zulhajji koranar Arfa koranar Idi izuwa ƙarshen kwanukan yanyane,) a bisa abinda Allah ya azurta musu na dabbobi, (iblu da bakaru da ganamu, raƙumi, saniya, tumakai waɗanda ake yankasu a ranar Idi da abinda yake bayansu na kyautayi da layya.) Kuci daga gareta (idan ta kasance mus'tahabbi ya. kuciyar da mai tsananin talauci
27. Sannan sukau da dauɗoɗinsu (da burwatse ɗin kansu, da tsawon farcensu,) su cika alwashensu (nadaga hadaya da layyoyi,) suyi Dawafi (Dawafin Ifala) da ɗaki daɗaɗɗe Be (domin shine farkon ɗakin da aka ajiye mabauta ga mutane.)

(HARAMCIN JIFAN JAMRATUL-AƘABATI DA TAKALMA DA ZAGINTA)

28. Al'amarin haka yake, wanda ya girmama alfarmace - alfarmacen shine abinda ketashi bai halattaba Allah, wannan girmamawan nan shine yafi amfani gareshi nan ga Ubangijinsa (a lahira,) an halatta muku dabbobi (acisu bayan yanka,) sai abinda ake karantawar haramcinsa a gareku (a cikin faɗin Ubangiji (Hurumat alaikumul-maitat) ku nisanci ƙazanta sune gumaka, ku nisanci shaidar zur (wato ƙarya dashirka a cikin Talbiya.)

1) Bayan ginin Annabi Ibrahimu saisu Amaliƙa, sai jurhumu sai ƙsaiyu, sai ƙuraishu sai juhairu sai hajjaju, ita ka'aba ayau ginin hajjajuce. Aƙarshe zamani Zul - wika'ataini zai rushe ta, Annabi Isa zai maida ita Allah ya kiyashemu da kiwonsa Amin.

حُنَفَآءَ لِلَّهِ غَيۡرَ مُشۡرِكِينَ بِهِۦۚ وَمَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَكَأَنَّمَا
خَرَّ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَتَخۡطَفُهُ ٱلطَّيۡرُ أَوۡ تَهۡوِي بِهِ ٱلرِّيحُ
فِي مَكَانٖ سَحِيقٖ ﴿31﴾ ذَٰلِكَۖ وَمَن يُعَظِّمۡ شَعَٰٓئِرَ ٱللَّهِ فَإِنَّهَا
مِن تَقۡوَى ٱلۡقُلُوبِ ﴿32﴾ لَكُمۡ فِيهَا مَنَٰفِعُ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمّٗى
ثُمَّ مَحِلُّهَآ إِلَى ٱلۡبَيۡتِ ٱلۡعَتِيقِ ﴿33﴾ وَلِكُلِّ أُمَّةٖ جَعَلۡنَا مَنسَكٗا لِّيَذۡكُرُواْ
ٱسۡمَ ٱللَّهِ عَلَىٰ مَا رَزَقَهُم مِّنۢ بَهِيمَةِ ٱلۡأَنۡعَٰمِۗ فَإِلَٰهُكُمۡ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞ
فَلَهُۥٓ أَسۡلِمُواْۗ وَبَشِّرِ ٱلۡمُخۡبِتِينَ ﴿34﴾ ٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِرَ ٱللَّهُ وَجِلَتۡ
قُلُوبُهُمۡ وَٱلصَّٰبِرِينَ عَلَىٰ مَآ أَصَابَهُمۡ وَٱلۡمُقِيمِي ٱلصَّلَوٰةِ
وَمِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ يُنفِقُونَ ﴿35﴾ وَٱلۡبُدۡنَ جَعَلۡنَٰهَا لَكُم مِّن شَعَٰٓئِرِ ٱللَّهِ
لَكُمۡ فِيهَا خَيۡرٞۖ فَٱذۡكُرُواْ ٱسۡمَ ٱللَّهِ عَلَيۡهَا صَوَآفَّۖ فَإِذَا وَجَبَتۡ
جُنُوبُهَا فَكُلُواْ مِنۡهَا وَأَطۡعِمُواْ ٱلۡقَانِعَ وَٱلۡمُعۡتَرَّۚ كَذَٰلِكَ
سَخَّرۡنَٰهَا لَكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ﴿36﴾ لَن يَنَالَ ٱللَّهَ لُحُومُهَا
وَلَا دِمَآؤُهَا وَلَٰكِن يَنَالُهُ ٱلتَّقۡوَىٰ مِنكُمۡۚ كَذَٰلِكَ سَخَّرَهَا لَكُمۡ
لِتُكَبِّرُواْ ٱللَّهَ عَلَىٰ مَا هَدَىٰكُمۡۗ وَبَشِّرِ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ﴿37﴾ ۞ إِنَّ ٱللَّهَ يُدَٰفِعُ
عَنِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ كُلَّ خَوَّانٖ كَفُورٍ ﴿38﴾

رُبع

29. Kuna masu totar don Allah ba masu shirkanta komai dashiba, duka wanda yayi shirka da Allah, to, haƙiƙa shi kamar ya faɗone daga sama akwai tsintsaye suka ƙauce shi ko iska ta fusgo shi ta silmanyo dashi a cikin guri mai nisa (daba a ƙaunar kuɓutarsa.)
30. Wannan (haka yake,) duka wanda ya girmama alamomin addinin Allah, haƙiƙa girmama tana daga tsoron Allah wanda yake cikin zukata.
31. Amfanunuwa na gareku a cikinta (kamar hawanta da ɗora mata kayan da bazai cuce taba,) izuwa lokaci abin ambato (lakacin soke ta,) sannan wurin halaccin soke ta, yana ga ɗaki mai 'yanta masu ziyara tasa.
32. Mun sanya mabauta ga kowace al'umma (data rigaya gabanku, wato gurin da zasuyi layya) domin su ambaci sunan Allah a bisa abinda ya azurta musu na daga marasa furuci na dabbobi (yayin yankanta,) to, Ubangijinku Allah ne makaɗaicin Sarki, to, kujawu izuwa gareshi shi kaɗai. Kayiwa masu kankandakai albishir.
33. Waɗanda idan an ambaci Allah zukatansu takan firgita, da masu dauriya a kan abinda ya samesu (nadaga bala'o'i,) da masu tsayar da salla (a cikin lokatanta) waɗanda suke ciyarwa daga abinda muka azurta musu.

(WANI ABU DAGA LADABAN YANKA A CIKIN HAJJI)

34. Manya-manyan busashe (wato raƙuma, mun sanyata) daga alamomin addinin Allah a gareku, amfani na gareku (a duniya a cikinta da lada a lahira,) to, ku ambaci sunan Allah a kanta yayin sukanta tana tsaye a kan kafafuwanta guda uku abar ɗaurewa hannun hagu, idan gyaffenta suka saraya izuwa ƙasa yimm!! bayan suka, to Kuci daga gareta in kun ga dama, kuciyar da mawadacin zuci wanda bai roƙa ba, bai nuna alamar roƙo bada wanda ya roƙa koya nuna alama, kamar irin wannan horewa ne muka hore muku ita a soketa a hauta. Ba don horewar Allah ba, baza a iya sarrafa ta ba, donku godewa ni'imata da nayi a gareku.
35. Namunta baya tarar da Ubangiji, hakana jininta, ba'a ɗagata izuwa gareshi saidai tsartsarkar niyyace take samunsa daga gareku, hakana ya hore muku ita domin ku girmama Allah donya shiryeku tafarkun addininku). Kayiwa masu kaɗaita Allah albishir.

(MUMINAN DA ALLAH YAKE MUSU YAKI KAMAR ANNABAWA DA WALIYYAI DA DUKKAN SALIHAI)

36. Haƙiƙa Ubangiji yana yaƙi gabarin waɗanda suka bada gaskiya, haƙiƙa Allah baya son mai yawancin amana, mai yawan butulci (ga ni'imar Allah).

أُذِنَ لِلَّذِينَ يُقَٰتَلُونَ بِأَنَّهُمْ ظُلِمُواْۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ نَصْرِهِمْ
لَقَدِيرٌ ﴿37﴾ ٱلَّذِينَ أُخْرِجُواْ مِن دِيَٰرِهِم بِغَيْرِ حَقٍّ إِلَّآ أَن يَقُولُواْ
رَبُّنَا ٱللَّهُۗ وَلَوْلَا دِفَٰعُ ٱللَّهِ ٱلنَّاسَ بَعْضَهُم بِبَعْضٍ
لَّهُدِّمَتْ صَوَٰمِعُ وَبِيَعٌ وَصَلَوَٰتٌ وَمَسَٰجِدُ يُذْكَرُ فِيهَا
ٱسْمُ ٱللَّهِ كَثِيرًاۗ وَلَيَنصُرَنَّ ٱللَّهُ مَن يَنصُرُهُۥٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَقَوِيٌّ عَزِيزٌ ﴿38﴾
ٱلَّذِينَ إِن مَّكَّنَّٰهُمْ فِي ٱلْأَرْضِ أَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُاْ ٱلزَّكَوٰةَ
وَأَمَرُواْ بِٱلْمَعْرُوفِ وَنَهَوْاْ عَنِ ٱلْمُنكَرِۗ وَلِلَّهِ عَٰقِبَةُ ٱلْأُمُورِ ﴿39﴾
وَإِن يُكَذِّبُوكَ فَقَدْ كَذَّبَتْ قَبْلَهُمْ قَوْمُ نُوحٍ
وَعَادٌ وَثَمُودُ ﴿40﴾ وَقَوْمُ إِبْرَٰهِيمَ وَقَوْمُ لُوطٍ ﴿41﴾ وَأَصْحَٰبُ
مَدْيَنَۖ وَكُذِّبَ مُوسَىٰ فَأَمْلَيْتُ لِلْكَٰفِرِينَ ثُمَّ أَخَذْتُهُمْۖ
فَكَيْفَ كَانَ نَكِيرِ ﴿42﴾ فَكَأَيِّن مِّن قَرْيَةٍ أَهْلَكْنَٰهَا
وَهِيَ ظَالِمَةٌ فَهِيَ خَاوِيَةٌ عَلَىٰ عُرُوشِهَا وَبِئْرٍ مُّعَطَّلَةٍ
وَقَصْرٍ مَّشِيدٍ ﴿43﴾ أَفَلَمْ يَسِيرُواْ فِي ٱلْأَرْضِ فَتَكُونَ لَهُمْ
قُلُوبٌ يَعْقِلُونَ بِهَآ أَوْ ءَاذَانٌ يَسْمَعُونَ بِهَاۖ فَإِنَّهَا لَا تَعْمَى
ٱلْأَبْصَٰرُ وَلَٰكِن تَعْمَى ٱلْقُلُوبُ ٱلَّتِي فِي ٱلصُّدُورِ ﴿44﴾

37. Anyi izni ga waɗannan da ake yaƙarsu (wato muminai) suma suyi yaƙi wannan Itace farkon aya data sauka a cikin yaƙi) saboda kafirai sun zaluncesu. Haƙiƙa Ubangiji lalle mai ikone bisa taimakonsu.

38. Sune waɗanda aka fitar dasu daga gidaddajinsu ba gaira badalilli sai wai kawai faɗinsu "Allah ne Ubangijinmu!" Badon ijewar Ubangiji mutane sashinsu da sashiba; da an rushe, hasumayoyi na masu bautar addinin Annabi Isa (Alaihis-salamu, Ruhban) wato da kanisoshinsu da kanisoshin Yahudu da abrananci sune salawatu waɗanda suke gaban zuwan Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama, amma bayan zuwansa dukkan wani addini bashiba ƙaryane) da masallatai na Musulmi da ake ambaton Allah da yawa a cikinsu (wato badon ƙarfin addinin Musulunci ba, da ba a bautawa Allah ba a cikin kowane lokaci.

(ALBISHIR GA JAMA'AR SUFAYE DA RINJAYE)

Lallai Allah zai taimaki wanda yake taimakon addininsa, (ba shakka Sufaye a kowane zamani su kaɗai ne suke taimakon addinin Allah, taimakon gaskiya). Haƙiƙa Ubangiji mai karfine (a kan halitta tasa) mabuwayine (a cikin mulkinsa").

39. Sune waɗanda in mun tabbatar dasu a cikin ƙasa (da taimakonsu kan magautansu) zasu tsayar da salla (da haƙƙoƙinta na zahiri da baɗini,) zasu bada zakka, za suyi umarni da aikin alheri, za suyi hani ga buran munkari. Kyakkyawan ƙarshe (na kowane lamari) ya tabbata ga Allah.

(IZNA DA WANDA YAGABATA NADAGA AL'UMMA)

40. Haƙiƙa idan sun ƙaryataka (Sallallahu alaika wasallama) to, haƙiƙa mutanen Annabi Nuhu (alaihissalamu) sun ƙaryatashi gabansu, da Ãdu (mutanen Annabi Huɗu alaihissalamu) da Samudu (mutanen Annabi Salihu alaihissalamu.)

41. Da mutanen Annabi Ibrahim (alaihissalamu) da mutanen Annabi Luɗu (alaihissalamu.)

42. Da abokan Madayana (mutanen Annabi Sha'aibu alaihissalamu) kuma ƙibɗawa sun ƙaryata Annabi Musa (alaihissalam, saboda haka sai kayi kwaikwayo da waɗannan Annabawa, rarrashine gareshi Sallallahu alaihi wasallama.) sainayi lamfa ga kafirai (wato najinkirta musu uƙuba) sannan na damƙesu. ƙaƙa damƙar da nayi musu? (Ya afku wurin afkuwarsa.)

43. Da yawa alƙarya muka halakar da ita, alhali tana mai zalunta ga kanta saboda kafirci,) ita mai faɗuwace a kan rumfuna Da yawa rijiya abar wofuntawa (saboda mutuwar masu ita) da katanga abar ɗaukakawa (sama, itama haka.)

44. Shin mutane basayi tafi yabane a ƙasa ya zama suna da zukata da suke hankaltan (abinda ya sauka ga waɗanda suke gabansu?) ko kunnuwa da suke jin (labaransu da halakarwa, suyi izna?) Haƙiƙa al'amarin idanduna ɓata makanta, kaidai zukata da suke cikin ƙiraza sune suke makanta.

وَيَسْتَعْجِلُونَكَ بِالْعَذَابِ وَلَن يُخْلِفَ اللَّهُ وَعْدَهُۥ وَإِنَّ يَوْمًا عِندَ
رَبِّكَ كَأَلْفِ سَنَةٍ مِّمَّا تَعُدُّونَ ﴿45﴾ وَكَأَيِّن مِّن قَرْيَةٍ
أَمْلَيْتُ لَهَا وَهِيَ ظَالِمَةٌ ثُمَّ أَخَذْتُهَا وَإِلَيَّ الْمَصِيرُ ﴿46﴾ * قُلْ
يَا أَيُّهَا النَّاسُ إِنَّمَا أَنَا لَكُمْ نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿47﴾ فَالَّذِينَ ءَامَنُوا
وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ لَهُم مَّغْفِرَةٌ وَرِزْقٌ كَرِيمٌ ﴿48﴾ وَالَّذِينَ
سَعَوْا فِي ءَايَاتِنَا مُعَاجِزِينَ أُولَٰئِكَ أَصْحَابُ الْجَحِيمِ ﴿49﴾
وَمَا أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ مِن رَّسُولٍ وَلَا نَبِيٍّ إِلَّا إِذَا تَمَنَّىٰ
أَلْقَى الشَّيْطَانُ فِي أُمْنِيَّتِهِۦ فَيَنسَخُ اللَّهُ مَا يُلْقِي الشَّيْطَانُ
ثُمَّ يُحْكِمُ اللَّهُ ءَايَاتِهِۦ وَاللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿50﴾ لِّيَجْعَلَ
مَا يُلْقِي الشَّيْطَانُ فِتْنَةً لِّلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٌ وَالْقَاسِيَةِ
قُلُوبُهُمْ وَإِنَّ الظَّالِمِينَ لَفِي شِقَاقٍ بَعِيدٍ ﴿51﴾ وَلِيَعْلَمَ
الَّذِينَ أُوتُوا الْعِلْمَ أَنَّهُ الْحَقُّ مِن رَّبِّكَ فَيُؤْمِنُوا بِهِۦ فَتُخْبِتَ لَهُۥ
قُلُوبُهُمْ وَإِنَّ اللَّهَ لَهَادِ الَّذِينَ ءَامَنُوا إِلَىٰ صِرَاطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿52﴾
وَلَا يَزَالُ الَّذِينَ كَفَرُوا فِي مِرْيَةٍ مِّنْهُ حَتَّىٰ تَأْتِيَهُمُ
السَّاعَةُ بَغْتَةً أَوْ يَأْتِيَهُمْ عَذَابُ يَوْمٍ عَقِيمٍ ﴿53﴾

ثمن

45. Suna neman gaggawarka da azaba, Allah baya saɓa alƙawarinsa, (ya damka musushi ranar Badar wato azaba.) Haƙiƙa wuninan ga Ubangijinka (daga kwanakin lahira) kamar shekara dubune daga abinda kuke kirgawa (na kwanukan duniya saboda tsananin azaba.)
46. Da yawa daga alƙarya da nayi mata lamfa, alhali tana azzaluma, sannan na damƙi mutanenta. Makomata tabbata zuwa gareni.

(MUHIMMANCIN AIKIN MANZANNI ALAIHIMUSSALAMU DA FALALAR IMANI DA AIKI NAGARI)

47. Faɗi (ya Annabi Sallallahu alaika wasallama) "Yaku jama'ar Musulmi, haƙiƙa ni manzo ne mabayyanin (gargaɗi) a gareku".
48. To, waɗanda suka bada gaskiya suka aikata ayyuka nagari, gafara ta tabbata garesu da arziki maigirma shine (aljanna).

(ALBISHIR GA MISHAN DA MASU TAIMAKONSU DA RASHIN NASARA DA TABEWA GA KOKARCE-KOKARCEN BUCE HASKEN MUSULUNCI)

49. Waɗanda sukayi kici-kici (wato sukayi kaikawo) a cikin bata ayoyinmu (na ƙur'anı, suna masu gaji da al'ummar Annabi alaihissalam) wadancananka azabar wutar jahannama ta tabbata a garesu. (Allah ya kiyashemu, Amin.)

(KIRARI GA ALƘUR'ANI DA CEWA SHI LITTAFINE DA BA KOKWANTO A CIKINSA WATO (GAMGAM) WANDA BABU WANI ABU LABO LABOA CIKINSA

50. Bamu aiko gabanka wani manzo ba ko Annabi, Manzo wanda aka umarceshi da isar da aike ko Annabi wanda ba a umarceshi da isar da aike ba face idan yayi karatu shaiɗan saiya jefa a cikin halin karatunsa (ƙaryace - ƙaryace a cikin kunnuwan kafirai.) Sai Ubangiji ya kawar da abinda shaiɗan ya jefa a cikin kunnuwan kafiran nan, (saboda Musulmi da ma basuji wannan ƙaryace-ƙaryace ba.) Sannan Ubangiji ya inganta ayoyinsa, Ubangiji masanine (da ƙaryace-ƙaryacen nan na kafirai,) gwanine (a cikin ɓata waɗannan ƙaryace- ƙaryace.)*
51. Donya sanya abinda shaiɗan yake jefawa (a cikin kunnuwan kafirai Ya sanyashi) fitina ga waɗanda munafunci yake cikin zukatansu da masu ƙeƙashashshiyar zuciya (wato mushirkai waɗanda shaiɗan ya jefa musu waɗannan ƙaryace-ƙaryace a cikin kunnuwansu,) haƙiƙa waɗannan kafirai (waɗanda shaiɗan ya jefa musu wannan ƙarya) suna cikin saɓani mai nisa (ga buran gaskiya).
52. kuma saboda waɗanda aka basu ilimi (na Tauhidi da Alƙur'ani sune Sahabban Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama waɗanda shaiɗan bai jefa musu komai a kunnuwansu ba,) su tabbatacewa shi Alƙur'ani gaskiya ne daga Ubangijinka, su dauwama kan bada gaskiya dashi, zukatansu ta nutsu dashi, haƙiƙa Ubangiji mai shiryar da waɗanda suka bada gaskiya ne tafarki madaidaici (addinin Musulunci.)
53. Waɗanda suka kafirta bazasu gushe basuna cikin kokwanto daga Alƙur'anı (saboda ƙaryace-ƙaryace da shaiɗan ya jefa a kunnuwansu) har alƙiyama tazo musu dim! (bada tanadi ba,) ko azabar rana bakarara tazo musu (Itace ranar (alƙiyama.)

*(To, wannan aya an sami magana a cikin Tafsirin Shehu Mahalli na zancen Garaniƙu, to, wannan Hadisi ƙarya akayiwa Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama, saboda haka ban fassara wannan aya da abinda Shehu Mahalli ya fassarata ba, na Hadisin Garaniƙu, saboda Allah bazai sallaɗa shaiɗan a kan Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama ba har ya jefa masa saɓo a kan harshensa a halin isar da aike, gashı kuma Ubangiji yana cewa, Waliyyaina bakada tasiri a kansu, to, barefa Annabawa alaihimussalamu, bare kuma Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama shugaban dukkan talikai.Saboda haka ina kiran dukkan Musulmi masu karanta tafsiri dasu dogara da abinda aka faɗa a nan, kadasu yarda da Hadisin Garaniƙu, don zindiƙaine suka girbawa Annabi Sallallahu alaihi wasallama ƙarya suka danganata gareshi, muna neman tsari da Allah. (A duba sawii.)

ٱلْمُلْكُ يَوْمَئِذٍ لِّلَّهِ يَحْكُمُ بَيْنَهُمْ فَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟
ٱلصَّٰلِحَٰتِ فِى جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ﴿٥٤﴾ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ وَكَذَّبُوا۟
بِـَٔايَٰتِنَا فَأُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمْ عَذَابٌ مُّهِينٌ ﴿٥٥﴾ وَٱلَّذِينَ هَاجَرُوا۟
فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ثُمَّ قُتِلُوٓا۟ أَوْ مَاتُوا۟ لَيَرْزُقَنَّهُمُ ٱللَّهُ
رِزْقًا حَسَنًا وَإِنَّ ٱللَّهَ لَهُوَ خَيْرُ ٱلرَّٰزِقِينَ ﴿٥٦﴾ لَيُدْخِلَنَّهُم
مُّدْخَلًا يَرْضَوْنَهُۥ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَعَلِيمٌ حَلِيمٌ ﴿٥٧﴾ * ذَٰلِكَ
وَمَنْ عَاقَبَ بِمِثْلِ مَا عُوقِبَ بِهِۦ ثُمَّ بُغِىَ عَلَيْهِ
لَيَنصُرَنَّهُ ٱللَّهُ إِنَّ ٱللَّهَ لَعَفُوٌّ غَفُورٌ ﴿٥٨﴾
ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ يُولِجُ ٱلَّيْلَ فِى ٱلنَّهَارِ وَيُولِجُ ٱلنَّهَارَ
فِى ٱلَّيْلِ وَأَنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌۢ بَصِيرٌ ﴿٥٩﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ
هُوَ ٱلْحَقُّ وَأَنَّ مَا يَدْعُونَ مِن دُونِهِۦ هُوَ
ٱلْبَٰطِلُ وَأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْعَلِىُّ ٱلْكَبِيرُ ﴿٦٠﴾
أَلَمْ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَتُصْبِحُ ٱلْأَرْضُ
مُخْضَرَّةً إِنَّ ٱللَّهَ لَطِيفٌ خَبِيرٌ ﴿٦١﴾ لَّهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَهُوَ ٱلْغَنِىُّ ٱلْحَمِيدُ ﴿٦٢﴾

رُبع

54. Sarauta a wannan rana ta Allah ce, yana hukunci, tsakanin muminai da kafirai (da abinda zai ambata mana a yanzu,) to, waɗanda suka bada gaskiya sukayi ayyuka nagargaru, suna cikin aljannatai na ni'ima (don falala daga Allah.)
55. Waɗanda suka kafirta suka ƙaryata da ayoyinmu, to, waɗancananka azaba mai wulaƙantarwa ta tabbata garesu.

(FALALAR HIJIRA SABODA ALLAH DA KIDIDDIGE NI'IMOMIN ALLAH GAREMU)

56. Waɗannan da sukayi hijira (cikin ɗa'ar Allah daga Makka zuwa Madina ko izuwa wani wuri,) sannan aka kashe su ko suka mutu, lallai Allah zai azurta su arziki mai kyau, (aljanna). Haƙiƙa Ubangiji lallai shine fiyayyen mai azurtawa.
57. Wallahi zai shigar dasu mashiga da zai yarda dashi (shine aljanna.) Haƙiƙa Ubangiji masanine (da niyyoyinsu,) mai jinkirin azabane (gawanda ya cancanceta.)
58. Al'amarin da muka baka labari haka yake, wanda yayi sakayya (na daga muminai) da gwargwadon abinda aka zalunceshi dashi sannan aka zalunceshi a kansa, (da fitar dashi daga gidansa bayan an yaƙeshi', ya yaƙesu a cikin wata mai alfarma,) lallai Allah zai taimake shi. Haƙiƙa Ubangiji mai rangwamene (ga muminai) mai gafara ne (garesu.)
59. Wannan nasara kuwa saboda cewa haƙiƙa Ubangiji yana shigarda dare cikin rana, yana shigar da rana cikin dare, haƙiƙa Ubangiji mai jin addu'ar muminai ne, mai ganinsune.
60. Wancananka (nasara haryau,) saboda cewa lallai Ubangiji shine tabbatacci kuma haƙiƙa abinda suke bautawa ba Allah ba, (sune gumaka,) shine balbaltacce, haƙiƙa Ubangiji shine maɗaukaki bisa komai, maigirma (wanda komai kankanine saishi.)
61. Shin bakayi sani ba, haƙiƙa Ubangiji ya saukar da ruwa daga sama ƙasa ta zama kore shar (wato makoranciya da tsirrai?) Kuma haƙiƙa Ubangiji mai tausasawane (da bayinsa a cikin fitar da iri da ruwa ko fitar da mutum daga cikin mahaifa ko waninsa,) masanine (da abinda yake cikin zukatansu yayin jinkirin ruwa ko waninsa)
62. Abinda yake sammai da ƙassaina ga Ubangiji (mallakarsa ce,) haƙiƙa Ubangiji lallai shine mawadaci (gaburan bayinsa,) abin godewa (ga waliyyansa.)

أَلَمْ تَرَ أَنَّ اللَّهَ سَخَّرَ لَكُم مَّا فِي الْأَرْضِ وَالْفُلْكَ تَجْرِي
فِي الْبَحْرِ بِأَمْرِهِ وَيُمْسِكُ السَّمَا أَن تَقَعَ عَلَى الْأَرْضِ
إِلَّا بِإِذْنِهِ إِنَّ اللَّهَ بِالنَّاسِ لَرَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿63﴾ وَهُوَ الَّذِي أَحْيَاكُمْ
ثُمَّ يُمِيتُكُمْ ثُمَّ يُحْيِيكُمْ إِنَّ الْإِنسَانَ لَكَفُورٌ ﴿64﴾
لِكُلِّ أُمَّةٍ جَعَلْنَا مَنسَكًا هُمْ نَاسِكُوهُ فَلَا يُنَازِعُنَّكَ فِي الْأَمْرِ
وَادْعُ إِلَىٰ رَبِّكَ إِنَّكَ لَعَلَىٰ هُدًى مُّسْتَقِيمٍ ﴿65﴾ وَإِن جَادَلُوكَ
فَقُلِ اللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا تَعْمَلُونَ ﴿66﴾ اللَّهُ يَحْكُمُ
بَيْنَكُمْ يَوْمَ الْقِيَامَةِ فِيمَا كُنتُمْ فِيهِ تَخْتَلِفُونَ ﴿67﴾
ثمن
* أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ اللَّهَ يَعْلَمُ مَا فِي السَّمَاءِ وَالْأَرْضِ إِنَّ ذَٰلِكَ فِي كِتَابٍ
إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى اللَّهِ يَسِيرٌ ﴿68﴾ وَيَعْبُدُونَ مِن دُونِ اللَّهِ
مَا لَمْ يُنَزِّلْ بِهِ سُلْطَانًا وَمَا لَيْسَ لَهُم بِهِ عِلْمٌ وَمَا لِلظَّالِمِينَ
مِن نَّصِيرٍ ﴿69﴾ وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمُ ءَايَاتُنَا بَيِّنَاتٍ تَعْرِفُ فِي وُجُوهِ
الَّذِينَ كَفَرُوا الْمُنكَرَ يَكَادُونَ يَسْطُونَ بِالَّذِينَ يَتْلُونَ
عَلَيْهِمْ ءَايَاتِنَا قُلْ أَفَأُنَبِّئُكُم بِشَرٍّ مِّن ذَٰلِكُمُ النَّارُ
وَعَدَهَا اللَّهُ الَّذِينَ كَفَرُوا وَبِئْسَ الْمَصِيرُ ﴿70﴾

63. Shin baka sani ba cewa haƙiƙa Allah ne ya hore muku abinda yake cikin ƙasa (nadaga dabbobi da motoci da jiragen ƙasa da makamantansu) ya hore muku komai (wato jirgin ruwa) tana gudu cikin kogi (da mahaya da kaya) da iznin Ubangiji, shine ya riƙe sama daga ta ruguzo a kan ƙasa, saida izininsa (ya zama ku halaka, haƙiƙa Ubangiji mai tsananin jinƙai ne (da mutane) mai rahamane (garesu a cikin horewar nan da riƙewar nan).

64. Shine wanda ya rayaku (da tsirar da ku,) sannan yake karɓar ranku (yayin ƙarewar ajalinku, sannan yake raYaku yayin tashin alƙiyama) haƙiƙa mutum mai yawan butulcine (ga ni'imomin Ubangiji.)

(KOWACE AL'UMMA TANA DA SHARI'A WACCE TA DACE DA ITA)

65. Mun sanya shari'a ga kowace al'umma daza suyi aiki da ita, sudaina jayyaya dakai cikin al'amarin (yanka, Don sunce wai abinda Allah ya kashe shi yafi cancanta da aci daga abinda mutum ya kashe. Yikira izuwa addinin Ubangijinka,) haƙiƙa kai kana kan addini madaidaici.

66. Idan sun yi jayayya dakai (a cikin lamarin addini, cene; "Allah ne masani da abinda kuke aikatawa (wannan tun gaban umarnine da yaƙi.)

67. Allah yana hukunci tsakaninku (ku muminai da kafirai) ranar alƙiyama a cikin abinda kuka kasance kuna sassaɓawa (a cikinsa).

68. Shin baka sani bane cewa Ubangiji yasan abinda yake cikin sammai da ƙassai? Haƙiƙa wancananka yana cikin Lauhul-Mahfuzu, haƙiƙa wancananka (abinda aka ambata) mai saukine bisa Allah.

(SASHIN AIKACE-AIKACEN KAFIRAI DA MUSHRIKAI)

69. Mushrikai suna bautawa abinda Allah bai saukar da hujja ga bauta tasaba na wanin Allah, (sune gumaka) da abinda basuda sani ɗashi (cewa ita iyayen gijice,) azzalumai basuda mai taimako dazai hana musu azabar Allah.

70. Idan ana karantawar ayoyinmu (na ƙur'ani) a garesu halin kasancewarsu mabayyana, kana shaida rashin yarda a cikin zukatan waɗanda suka kafirta (ta wajen murtuke fuska) suna kusa suyi tumbi ga waɗanda suke karanta musu ayoyinmu a garesu, cene; Shin, "to, bana baku labari da mafi sharri daga wancananku ba, (wato mafi muni gareku daga alƙur'anin da ake karantawa gareku) Itace wutada Allah ya alƙawartata ga waɗanda suka kafirta, tur da makoma ita.

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ضُرِبَ مَثَلٌ فَٱسْتَمِعُواْ لَهُۥٓ إِنَّ ٱلَّذِينَ
تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ لَن يَخْلُقُواْ ذُبَابًا
وَلَوِ ٱجْتَمَعُواْ لَهُۥ وَإِن يَسْلُبْهُمُ ٱلذُّبَابُ شَيْـًٔا لَّا يَسْتَنقِذُوهُ مِنْهُ
ضَعُفَ ٱلطَّالِبُ وَٱلْمَطْلُوبُ ﴿٧١﴾ مَا قَدَرُواْ ٱللَّهَ حَقَّ
قَدْرِهِۦٓ إِنَّ ٱللَّهَ لَقَوِىٌّ عَزِيزٌ ﴿٧٢﴾ ٱللَّهُ يَصْطَفِى
مِنَ ٱلْمَلَٰٓئِكَةِ رُسُلًا وَمِنَ ٱلنَّاسِ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌۢ
بَصِيرٌ ﴿٧٣﴾ يَعْلَمُ مَا بَيْنَ أَيْدِيهِمْ وَمَا خَلْفَهُمْ وَإِلَى ٱللَّهِ
تُرْجَعُ ٱلْأُمُورُ ﴿٧٤﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱرْكَعُواْ
وَٱسْجُدُواْ وَٱعْبُدُواْ رَبَّكُمْ وَٱفْعَلُواْ ٱلْخَيْرَ لَعَلَّكُمْ
تُفْلِحُونَ ۩ ﴿٧٥﴾ وَجَٰهِدُواْ فِى ٱللَّهِ حَقَّ جِهَادِهِۦ
هُوَ ٱجْتَبَىٰكُمْ وَمَا جَعَلَ عَلَيْكُمْ فِى ٱلدِّينِ مِنْ حَرَجٍ
مِّلَّةَ أَبِيكُمْ إِبْرَٰهِيمَ هُوَ سَمَّىٰكُمُ ٱلْمُسْلِمِينَ مِن قَبْلُ
وَفِى هَٰذَا لِيَكُونَ ٱلرَّسُولُ شَهِيدًا عَلَيْكُمْ وَتَكُونُواْ
شُهَدَآءَ عَلَى ٱلنَّاسِ فَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُواْ ٱلزَّكَوٰةَ
وَٱعْتَصِمُواْ بِٱللَّهِ هُوَ مَوْلَىٰكُمْ فَنِعْمَ ٱلْمَوْلَىٰ وَنِعْمَ ٱلنَّصِيرُ ﴿٧٦﴾

(SANYA MISALI DON A GANE)

71. Yaku mutane an sanya misali ku saurare shi, (shine) wađannan dakuke bautawa ba Allah ba (sune gumaka) bazasu iya halittar ƙudaba kodasun tattara don halittar, idan ƙuda ya karɓe musu wani abu (nadaga turare da za'afaran wanda suke shafawa gumakan) bazasu iya ƙwatoshi daga wurinsa ba (saboda gajiyawarsu,) mai bauta da abin bautawa sun raunana (wato haihuwar guzuma kenan đa kwance uwa kwance inji hausawa).

72. Basu girmama Allah ba gwargwadon girmansa (daya kamaceshi, Don sun , tara dashi abinda bai hanu ga buran ƙudaba, bakuma zai iya ƙwato wani abu daga ƙuda ba idan ya tsotsa.) Haƙiƙa Ubangiji mai ƙarfine mai rinjaye.

73. Ubangiji yana zaɓin manzanni daga Mala'iku, kuma yana zaɓin manzanni daga mutane, (ta sauka yayin da mushrikai Sukace, Shin a saukar masa da alƙur'ani a tsakaninmu?) Ubangiji mai jin zancensune mai ganine (ga wanda zai riƙeshi manzo kamar Jibrila da Mika'ila da Ibrahima da Muhammadu da waninsu Sallallahu alaihim wasallama.

74. Yasan abinda yake gabansu da abinda yake bayansu (da abinda suka gabatar da abinda suka jinkirtar da abinda zasu aikata a gaba,) izuwa ga Allah ake komar da al'amura.

(SHARI'AR MUSULUNCI A MULMULE)

75. Yaku wađanda suka bada gaskiya, kuyi sunkuyan salla ku dungura goshi, ku kađaita Ubangijinku, ku aikata alheri (kamar sadar da zumuntada Maka-rimul-ahlaƙi da waninsa,) don ku sami rabauta (da aljanna.)

76. Kuyi yaƙi saboda Allah (don tsaida addininsa,) kubada matuƙar ƙoƙarinku a cikin yaƙin, Allah ne ya zaɓeku ga addininsa, bai sanya muku ƙunci cikin addini ba, (Ya sawwake muku su yayin tsanani kamar ƙasaru da taimama dacin mushe da shan azumi saboda rashin lafiya da tafiya,) Madalla addinin ubanku Annabi Ibrahimu (alaihissalamu) Allah ne ya ambace ku Musulmai gaban (wannan littafi,) kuma ya ambaceku Musulmai cikin wannan littafi (alƙur'ani) don Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama) ya kasance shaida a kanku (ranar alƙiyama, cewa ya iyar muku,) kuma ku zama shaidu a kan mutane,(cewa ma'aikansu sun iyar musu.) To, ku dauwama bisa tsaida salla (kamar yadda ya kamata,) ku bada zakka, ku amince da Allah, shine mataimakinku, to, madalla mataimaki (Allah!) Madalla mai agaji a gareku (Allah!!)

23 سُورَةُ المُؤْمِنُونَ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ مِائَةٌ وَتِسْعَ عَشْرَةَ آيَةً 119

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

حزب

* قَدْ أَفْلَحَ الْمُؤْمِنُونَ (1) الَّذِينَ هُمْ فِي صَلَاتِهِمْ خَاشِعُونَ (2) وَالَّذِينَ
هُمْ عَنِ اللَّغْوِ مُعْرِضُونَ (3) وَالَّذِينَ هُمْ لِلزَّكَاةِ فَاعِلُونَ (4)
وَالَّذِينَ هُمْ لِفُرُوجِهِمْ حَافِظُونَ (5) إِلَّا عَلَىٰ أَزْوَاجِهِمْ أَوْ مَا مَلَكَتْ
أَيْمَانُهُمْ فَإِنَّهُمْ غَيْرُ مَلُومِينَ (6) فَمَنِ ابْتَغَىٰ وَرَاءَ ذَٰلِكَ فَأُولَٰئِكَ هُمُ
الْعَادُونَ (7) وَالَّذِينَ هُمْ لِأَمَانَاتِهِمْ وَعَهْدِهِمْ رَاعُونَ (8) وَالَّذِينَ هُمْ
عَلَىٰ صَلَوَاتِهِمْ يُحَافِظُونَ (9) أُولَٰئِكَ هُمُ الْوَارِثُونَ (10) الَّذِينَ يَرِثُونَ
الْفِرْدَوْسَ هُمْ فِيهَا خَالِدُونَ (11) وَلَقَدْ خَلَقْنَا الْإِنْسَانَ مِنْ سُلَالَةٍ
مِنْ طِينٍ (12) ثُمَّ جَعَلْنَاهُ نُطْفَةً فِي قَرَارٍ مَكِينٍ (13) ثُمَّ خَلَقْنَا النُّطْفَةَ عَلَقَةً
فَخَلَقْنَا الْعَلَقَةَ مُضْغَةً فَخَلَقْنَا الْمُضْغَةَ عِظَامًا فَكَسَوْنَا الْعِظَامَ
لَحْمًا ثُمَّ أَنْشَأْنَاهُ خَلْقًا آخَرَ فَتَبَارَكَ اللَّهُ أَحْسَنُ الْخَالِقِينَ (14)
ثُمَّ إِنَّكُمْ بَعْدَ ذَٰلِكَ لَمَيِّتُونَ (15) ثُمَّ إِنَّكُمْ يَوْمَ الْقِيَامَةِ تُبْعَثُونَ (16)
وَلَقَدْ خَلَقْنَا فَوْقَكُمْ سَبْعَ طَرَائِقَ وَمَا كُنَّا عَنِ الْخَلْقِ غَافِلِينَ (17)

Suratul-Muminina

A Makka Aka. Saukar Da Ita (gaban Hijira) Ayoyinta Dari Da Goma Sha Tara (119)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabaɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

(WANNAN SURA TA ƘUNSHI IMANI DA MUMINAI WATO TANA MAGANA KAN MUMINI TAMMI! DA HALU-LUWAN DASUKE RARRABE SHI DAGA WANINSA, WANNAN SURA CE BABBA A WURINMU WACCE TA NUNA CEWA MUMINI YANADA MARTABA WURIN UBANGIJI WACCE UBANGIJI YAYI MASA KIRARI DA KYAWAWAN KAMBI WAƊANDA ALLAH YA KWAFA A KAN MUMINI NA DAUKAKAR MARTABA A DUNIYA DA LAHIRA)

(Sufofin Muminai)

1. Haƙiƙa muminai sun rabauta.
2. Waɗandasune masu ƙanƙandakai a cikin sallarsu.
3. Da waɗandasune masu bujirewa ga barin zancen banza.
4. Da waɗandasune masu miƙawa da zakka, (wato masu bada zakka).
5. Waɗanda sune masu kiyayewa ga farjojinsu.
6. Saiko ga matayensu ko abinda hannunsu ta mallaka (na daga ƙwaraƙwarai,) haƙiƙa su ba ababan zargi bane (a cikin saduwa dasu).
7. To, duka wanda ya nemi wanin wancananka mataye da kwara-kwarai (kamar fitar da maniyyi da hannu, ko wani abu daban kamar haka,) to, haƙiƙa waɗancananka sune masu shisshigi"
8. Da waɗandasune masu kiyayewa ga amanoninsu da alƙawuransu (cikin abinda yake tsakaninsu da Allah ko da mutane).
9. Da waɗandasune masu dauwama a kan sallolinsu (a cikin lokatanta wato suna bada kowace salla a farkon lokatanta).
10. Waɗancananka haƙiƙa sune kaɗai magada.
11. Waɗanda suke gadon aljannar Firdausi su madawwama ne a cikinta.

(ASALIN 'YAN ADAM TAREDA GWANINTAR ALLAH)

12. Haƙiƙa Ubangiji ya halicci mutum (Annabi Adamu alaihissalamu) daga dallaki na yunɓu,
13. Sannan muka sanyashi maniyyi a cikin matabbace amintacce (Itace mahaifa).
14. Sannan muka mayar da ita nuɗufar nan jini sandararre, sannan muka halicci jinin nan muka mayar dashi tsoka, (gwargwadon daza a iya taunawa) sannan muka tufasar da ƙasusuwan nan nama, sannan muka fareshi wata irin halitta dabam, da busa rai a cikinsa, Kai! Ubangiji mafi gwanintar gwanaye ya girma, alherinsa ya daɗu ya yawaita!
15. Sannan kuma ku, lalle zaku mutu bayan wancananka.
16. Sannan haƙiƙa ku, ranar alƙiyama za a tasheku (don sakamako).
17. Haƙiƙa mun halicci sammai bakwai burbushinku (wato tafarkun Mala'iku,) bamu kasance marabkana ga barin halittu dake ƙarƙashinta ba, (wato sama ta ruguzo musu su halaka. Kai! Muna riƙesu bazasu ruguzo ba).

وَأَنزَلْنَا مِنَ السَّمَاءِ مَاءً بِقَدَرٍ فَأَسْكَنَّاهُ فِي الْأَرْضِ وَإِنَّا عَلَىٰ
ذَهَابٍ بِهِ لَقَادِرُونَ ﴿18﴾ فَأَنشَأْنَا لَكُم بِهِ جَنَّاتٍ مِّن نَّخِيلٍ وَأَعْنَابٍ
لَّكُمْ فِيهَا فَوَاكِهُ كَثِيرَةٌ وَمِنْهَا تَأْكُلُونَ ﴿19﴾ وَشَجَرَةً تَخْرُجُ
مِن طُورِ سَيْنَاءَ تَنبُتُ بِالدُّهْنِ وَصِبْغٍ لِّلْآكِلِينَ ﴿20﴾ * وَإِنَّ لَكُمْ
فِي الْأَنْعَامِ لَعِبْرَةً نُّسْقِيكُم مِّمَّا فِي بُطُونِهَا وَلَكُمْ فِيهَا مَنَافِعُ
كَثِيرَةٌ وَمِنْهَا تَأْكُلُونَ ﴿21﴾ وَعَلَيْهَا وَعَلَى الْفُلْكِ تُحْمَلُونَ ﴿22﴾
وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوْمِهِ فَقَالَ يَا قَوْمِ اعْبُدُوا اللَّهَ
مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُ أَفَلَا تَتَّقُونَ ﴿23﴾ فَقَالَ الْمَلَأُ الَّذِينَ كَفَرُوا
مِن قَوْمِهِ مَا هَٰذَا إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ يُرِيدُ أَن يَتَفَضَّلَ عَلَيْكُمْ وَلَوْ شَاءَ اللَّهُ
لَأَنزَلَ مَلَائِكَةً مَّا سَمِعْنَا بِهَٰذَا فِي آبَائِنَا الْأَوَّلِينَ ﴿24﴾ إِنْ هُوَ
إِلَّا رَجُلٌ بِهِ جِنَّةٌ فَتَرَبَّصُوا بِهِ حَتَّىٰ حِينٍ ﴿25﴾ قَالَ رَبِّ
انصُرْنِي بِمَا كَذَّبُونِ ﴿26﴾ فَأَوْحَيْنَا إِلَيْهِ أَنِ اصْنَعِ الْفُلْكَ
بِأَعْيُنِنَا وَوَحْيِنَا فَإِذَا جَاءَ أَمْرُنَا وَفَارَ التَّنُّورُ فَاسْلُكْ فِيهَا
مِن كُلٍّ زَوْجَيْنِ اثْنَيْنِ وَأَهْلَكَ إِلَّا مَن سَبَقَ عَلَيْهِ الْقَوْلُ
مِنْهُمْ وَلَا تُخَاطِبْنِي فِي الَّذِينَ ظَلَمُوا إِنَّهُم مُّغْرَقُونَ ﴿27﴾

ثمن

18. Hakika mun saukar da ruwa daga sama, da gwargwadon (isuwar mutane,) Muka tsareshi a cikin ƙasa, hakika Mu lalle masu ikone a bisa tafiya dashi, (su mutu tareda dabbobinsu don ƙishirwa).
19. Muka farar muku gonakai dashi, na dabinai da inabai, ababan marmari na gareku a cikinta masu yawa, kuma kunaci daga gareta (damuna da rani).
20. Muka tsirad da itaciya wacce take fitowa daga ɗurusina, tana tsuro da mai (wato Itace itaciyar Zaituni), da kuma rini ga masu cin abinci (wato miya da ake tsomowa ta rina loma).
21. Hakika kuna da izina a cikin dabbobi (raƙuma da shanu da tumakai,) muna sha daku ,nono daga abinda yake cikin cukkunansu, kuna da amfanuwa masu yawa (na daga lallausan gashin raƙumi dana tumakai da dukkan gasu,) kuma kunaci daga gareta.
22. Ana ɗauke daku ,akanta da kuma kan jiraga.

(LABARIN ANNABI NUHU ALAIHISSALAMU DA ABINDA YA ƘUNSA NA DAGA GARGADI)

23. Hakika mun aiko Annabi Nuhu (Alaihissalamu) izuwa mutanensa, yace, "Yaku mutanena ku bautawa Allah ku kaɗai ta shi, bakuda wani abin bautawa waninsa, shin ba kwa ji tsoron Ubangiji ba (ku ɗena bautar waninsa?")
24. To, manyan mutane waɗanda suka kafirta na daga mutanensa sukace (ga mabiyansu), "Wannan bai kasance ba, (wato Annabi Nuhu Alaihissalamu) face mutumne kamarku, yana nufin yafifita a kanku (wato ya danneku, yazama shugabanku ku zama mabiyansa,) da Allan ya nufi (kada a bautawa waninsa) da saiya saukar da Mala'iku (ba mutum ba,) bamu taba jin wannan abu da Nuhu ya kirawo mu izuwa gareshi na tauhidi ba a cikin iyayenmu na farko.
25. "Shi Annabi Nuhu bai kasance ba face mutumne da hauka yake tare dashi, kuyi sauraro dashi har izuwa lokacin mutuwarsa".
26. Annabi Nuhu (Alaihissalamu) yace, "Ubangijina taimakan ni a kansu Don sun ,ƙaryatani, (wato halakar dasu)."
27. Ubangiji ya faɗa (yana mai amsa addu'arso) akansu "Sai muka aiko izuwa gareshi cewa ka sassaƙa jirgi da kulawarmu, da alƙawarmu, to, idan umarninmu yazo (da halakar dasu,) tanderu ya kece (da ruwa , wannan alamace ga Annabi Nuhu alaihissalamu,) saika shigar da biyu a cikin jirgin daga dukkan aure biyu, (namiji da mace daga kowane nau'insu, a cikin ƙissa, Ubangiji ya tara namun jeji ga Annabi Nuhu alaihissalamu, da waninsu ya haɗu yana sanya hannayensa a cikin kowane nau'i, sai hannunsa ta dama ta auku kan namiji, ta hagu ta auku kan tamata, saiya sakasu a cikin jirgin nasa) ka shigar kuma da iyalinka, (wato matarka da 'ya'yanka,) sai wanda magana ta rigaya a garesu (da halakarwa, sune mata tasa da ɗansa Kan'anu, sabanin Samu da Hamu dayafisu, ya ɗaukesu da matayensu guda uku, Ance duka waɗanda suka kasance cikin jirgin nan su saba'in da takwas (78), rabin su maza ne rabi kuma mata), kada kayi min magana cikin waɗanda suka zalinci kansu (da kafirci, da barin halakar dasu,) hakika su ababan nutsarwa ne.

فَإِذَا ٱسْتَوَيْتَ أَنتَ وَمَن مَّعَكَ عَلَى ٱلْفُلْكِ فَقُلِ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ
ٱلَّذِى نَجَّىٰنَا مِنَ ٱلْقَوْمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿28﴾ وَقُل رَّبِّ أَنزِلْنِى مُنزَلًا
مُّبَارَكًا وَأَنتَ خَيْرُ ٱلْمُنزِلِينَ ﴿29﴾ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ وَإِن كُنَّا
لَمُبْتَلِينَ ﴿30﴾ ثُمَّ أَنشَأْنَا مِنۢ بَعْدِهِمْ قَرْنًا ءَاخَرِينَ ﴿31﴾
فَأَرْسَلْنَا فِيهِمْ رَسُولًا مِّنْهُمْ أَنِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مَا لَكُم
مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥٓ أَفَلَا تَتَّقُونَ ﴿32﴾ وَقَالَ ٱلْمَلَأُ مِن قَوْمِهِ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ وَكَذَّبُوا۟ بِلِقَآءِ ٱلْءَاخِرَةِ وَأَتْرَفْنَٰهُمْ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا مَا هَٰذَآ
إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ يَأْكُلُ مِمَّا تَأْكُلُونَ مِنْهُ وَيَشْرَبُ مِمَّا تَشْرَبُونَ ﴿33﴾ وَلَئِنْ
أَطَعْتُم بَشَرًا مِّثْلَكُمْ إِنَّكُمْ إِذًا لَّخَٰسِرُونَ ﴿34﴾ أَيَعِدُكُمْ أَنَّكُمْ إِذَا مِتُّمْ وَكُنتُمْ
تُرَابًا وَعِظَٰمًا أَنَّكُم مُّخْرَجُونَ ﴿35﴾ * هَيْهَاتَ هَيْهَاتَ لِمَا تُوعَدُونَ ﴿36﴾ رُبْع
إِنْ هِىَ إِلَّا حَيَاتُنَا ٱلدُّنْيَا نَمُوتُ وَنَحْيَا وَمَا نَحْنُ بِمَبْعُوثِينَ ﴿37﴾ إِنْ هُوَ
إِلَّا رَجُلٌ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا وَمَا نَحْنُ لَهُۥ بِمُؤْمِنِينَ ﴿38﴾ قَالَ رَبِّ ٱنصُرْنِى
بِمَا كَذَّبُونِ ﴿39﴾ قَالَ عَمَّا قَلِيلٍ لَّيُصْبِحُنَّ نَٰدِمِينَ ﴿40﴾
فَأَخَذَتْهُمُ ٱلصَّيْحَةُ بِٱلْحَقِّ فَجَعَلْنَٰهُمْ غُثَآءً فَبُعْدًا لِّلْقَوْمِ
ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿41﴾ ثُمَّ أَنشَأْنَا مِنۢ بَعْدِهِمْ قُرُونًا ءَاخَرِينَ ﴿42﴾

28. "Idan kayi daidai kai da wanda yake taredakai a kan wannan jirgi, to, sai kace" Godiya ta tabbata ga Allah, wanda ya tserar damu daga mutane kafirai.
29. "Kafaɗa (yayin saukarka daga jirgin nan, kace,) "Ya Ubangijina, saukar dani masauki mai albarka, haƙiƙa kaine fiyayyen masu saukarwa".

(IZNACE - IZNACE MASU NUNA IKON UBANGIJI)

30. Haƙiƙa akwai ıznace-iznace a cikin wancananka (abin ambato, shine al'amarin Annabi Nuhu alaihissalamu da jirgin da halakar da kafirai.) Haƙiƙa Mun Kasance masu jarrabar (mutanen Annabi Nuhu alaihissalamu, Muka aikoshi garesu).

(ƘISSAR ANNABI HUDU ALAIHISSA-LAM DA ABIN TA KUNSA NA MUMMUNAN KARSHE NA MASU HANNU-DA-SHUNI)

31. Sannan Muka fari waɗansu mutanen bayansu, (wato sune Adu).
32. Muka aiko manzo daga garesu (shine Annabi Hudu Alaihissalamu) cewa "Ku bautawa Allah, bakuda wani abin bautawa bashi ba. Shin ba kwa tsoraci Allah ba".
33. Manyan mutane daga jama'arsa, waɗanda suka kafirta suka ƙaryata tashin alƙiyama muka ni'imta su a cikin rayuwar duniya, Sukace, "Wannan bai kasance ba face mutumne kamar ku, yana ci daga abinda kuke ci gareshi, yana sha daga abinda kuke sha daga gareshi.
34. "Wallahi idan kuka bi mutum kamarku, haƙiƙa ku yayin nan lalle taɓaɓɓu ne ku".
35. "Yaya zai dinga baku tsoro cewa ku idan kun mutu kuka zama turɓaya da kasusuwa za a mayar da ku.
36."Kai! kai! akwai nisa kwarai da abinda ake muku ban tsoro dashi.
37. "Ita rayuwa bata kasance ba sai rayuwar mu ta duniya, mu mutu murayu (da rayuwar 'ya'yanmu,) mu baza a tashe mu (daga ƙaburbura ba).
38. "Wannan jaka da bai kasance basai mutumne daya kagi ƙarya bisa Ubangiji, mu bamu kasance masu gasgatawa dashi ba, (a cikin tashinmu bayan mutuwa").
39. Yace, "Ubangijina taimake ni Donsun , ƙaryata ni".
40. Ubangiji yace, bada daɗewa ba lalle zasu wayi gari suna masu nadama (a bisa kafircinsu da ƙaryatarwarsu").
41. Sai tsawar azaba tafar musu da gaskiya, (suka mutu,) muka mayar dasu tarkace, to, nisa daga rahamar Allah ta tabbata ga mutane azzalumai (masu karyatawan Annabi Sallallahu alaihi wasallama).

(AMBATON SASHIN ANNABAWA ALAIHIMUSSALAM)

42. Sannan muka fari waɗansu mutane bayansu, daban.

مَا تَسْبِقُ مِنُ اُمَّةٍ اَجَلَهَا وَمَا يَسْتَـْٔخِرُونَ ﴿43﴾ ثُمَّ أَرْسَلْنَا رُسُلَنَا
تَتْرَاۖ كُلَّمَا جَآءَ اُمَّةً رَّسُولُهَا كَذَّبُوهُۖ فَأَتْبَعْنَا بَعْضَهُم بَعْضاً
وَجَعَلْنَٰهُمُۥٓ أَحَادِيثَۖ فَبُعْداً لِّقَوْمٍ لَّا يُومِنُونَۖ ﴿44﴾ ثُمَّ أَرْسَلْنَا
مُوسَىٰ وَأَخَاهُ هَٰرُونَ ﴿45﴾ بِـَٔايَٰتِنَا وَسُلْطَٰنٍ مُّبِينٍ ﴿46﴾ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ
وَمَلَإِيْهِۦ فَاسْتَكْبَرُواْ وَكَانُواْ قَوْماً عَالِينَۖ ﴿47﴾ فَقَالُواْ أَنُومِنُ
لِبَشَرَيْنِ مِثْلِنَا وَقَوْمُهُمَا لَنَا عَٰبِدُونَۖ ﴿48﴾ فَكَذَّبُوهُمَا فَكَانُواْ
مِنَ ٱلْمُهْلَكِينَۖ ﴿49﴾ وَلَقَدَ اٰتَيْنَا مُوسَى ٱلْكِتَٰبَ لَعَلَّهُمْ
يَهْتَدُونَۖ ﴿50﴾ وَجَعَلْنَا ٱبْنَ مَرْيَمَ وَأُمَّهُۥٓ ءَايَةً وَءَاوَيْنَٰهُمَا إِلَىٰ رُبْوَةٍ
ذَاتِ قَرَارٍ وَمَعِينٍۖ ﴿51﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلرُّسُلُ كُلُواْ مِنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَاعْمَلُواْ صَٰلِحاً
إِنِّيَ بِمَا تَعْمَلُونَ عَلِيمٌۖ ﴿52﴾ وَأَنَّ هَٰذِهِۦٓ أُمَّتُكُمُۥٓ أُمَّةً وَٰحِدَةً وَأَنَا رَبُّكُمْ
فَاتَّقُونِۖ ﴿53﴾ فَتَقَطَّعُواْ أَمْرَهُم بَيْنَهُمْ زُبُراًۖ كُلُّ حِزْبِۢ بِمَا
لَدَيْهِمْ فَرِحُونَۖ ﴿54﴾ فَذَرْهُمْ فِے غَمْرَتِهِمْ حَتَّىٰ حِينٍۖ ﴿55﴾ أَيَحْسِبُونَ
أَنَّمَا نُمِدُّهُم بِهِۦ مِن مَّالٍ وَبَنِينَ ﴿56﴾ نُسَارِعُ لَهُمْ فِے ٱلْخَيْرَٰتِۖ بَل لَّا يَشْعُرُونَۖ ﴿57﴾
* إِنَّ ٱلَّذِينَ هُم مِّنْ خَشْيَةِ رَبِّهِم مُّشْفِقُونَ ﴿58﴾ وَٱلَّذِينَ هُم بِـَٔايَٰتِ ثمن
رَبِّهِمْ يُومِنُونَ ﴿59﴾ وَٱلَّذِينَ هُم بِرَبِّهِمْ لَا يُشْرِكُونَ ﴿60﴾

43. Babu wata al'umma da zata rigayi ajalinta baza kuma sujinkirceshi ba.
44. Sannan Muka aiko jakadunmu, masu bibiya (tsakanin kowane mutum biyu akwai zamani mai tsawo,) ko dayaushe jakadan al'umma yazo mata saisu ƙaryata shi, sai mu biyar da ba'alinsu ga ba'ali (a cikin halaka,) muka mayar dasu hirarraki, nisa daga rahamar Allah ya tabbata ga mutanen da basa bada gaskiya.
45. Sannan Muka aiko Annabi Musa da dan uwansa Annabi Haruna (alaihimussalam).
46. Da ayoyimnu da hujja mabayyahiya, (Itace sanda da hannu da waninsu),
47. Izuwa Fir'auna da manyan mutanensa, sukayi girman kai ga barin bada gaskiya da ita, sun kasance mutane ne masu rinjaye da zalunci.
48. Sukace, "Ma bada gaskiya don mutum biyu irinmu, alhalin mutanensu masu bauta ne garemu?"
49. Suka ƙaryata su, suka kasance daga cikin halakakku.
50. Haƙiƙa mun baiwa Annabi Musa (Alaihissalam) Attaura don mutanensa Bani-Isra'ila su shiriya (dashi daga ɓata, anbashi itane bayan halakar Fir'auna da mutanensa bakiɗaya).
51. Mun sanya Annabi Isa (dan Maryamu alaihissalamu) da mahaifiyarsa aya, (ta manaki, shine haihuwar sa batareda kusantar namiji ba,) Mun tattara su izuwa tudu, (wato Baitul-Maƙadisi ko Dimashƙa) ma'abuciyar daidaito, (mazauninta, yana zama daidai a kanta,) tareda ruwa mai gudu.

UMARNI WANDA AKAI DA CIN HA-LAL WANDA YA ƘUNSHI WAJABCINCIN HALAL DA AIKINA GARI WANDASHINE ASALIN SUFANCI

52. Yaku waɗannan manzanni, Kuci daga halaloli tsantsa mawofinta ga buran shubuhohi kuyi aiki na gari salloli farilla ko nafila, haƙiƙa Ni masanine da abinda kuke aikatawa.
53. Ku sani haƙiƙa wannan addini na Musulunci shine addiniku, addini guda daya, nine kuma Ubangijinku, kuji tsorona,
54. Sai suka yanyanka al'amarinsu daban dabankowace kungiya suna farin ciki da abinda ke garesu.
55. To, ka barsu (kafiran Makka,) a ciki batansu, har lokacin mutuwarsu.
56. Shinsa dinga zaton cewa abinda muke kiransu dashi na dukiya da 'ya'yaye (a duniya,)
57. Muna garaje ne dasu a cikin alheri, (A'a!) Kaidai basusan (cewa wannan maƙarƙashi yace ba).
58. Haƙiƙa waɗanda suke masu firgita saboda tsoron Ubangijinsu,
59. Da waƙandasuke masu bada gaskiya da ayoyin Ubangijinsu (wato Alƙur'ani),
60. Da waɗanda suke basa tara kowa da Ubangijinsu,

وَالَّذِينَ يُوتُونَ مَا ءَاتَوا وَّقُلُوبُهُمْ وَجِلَةٌ اَنَّهُمُ إِلَىٰ رَبِّهِمْ رَاجِعُونَ ﴿61﴾
أُوْلَٰٓئِكَ يُسَٰرِعُونَ فِي الْخَيْرَٰتِ وَهُمْ لَهَا سَٰبِقُونَ ﴿62﴾
وَلَا نُكَلِّفُ نَفْساً اِلَّا وُسْعَهَا وَلَدَيْنَا كِتَٰبٌ يَنطِقُ بِالْحَقِّ
وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿63﴾ بَلْ قُلُوبُهُمْ فِي غَمْرَةٍ مِّنْ هَٰذَا وَلَهُمُۥ أَعْمَٰلٌ مِّن
دُونِ ذَٰلِكَ هُمْ لَهَا عَٰمِلُونَ ﴿64﴾ حَتَّىٰ إِذَا أَخَذْنَا مُتْرَفِيهِم بِالْعَذَابِ
إِذَا هُمْ يَجْـَٔرُونَ ﴿65﴾ لَا تَجْـَٔرُوا الْيَوْمَ إِنَّكُم مِّنَّا لَا تُنصَرُونَ ﴿66﴾
قَدْ كَانَتْ ءَايَٰتِي تُتْلَىٰ عَلَيْكُمْ فَكُنتُمْ عَلَىٰ أَعْقَٰبِكُمْ تَنكِصُونَ ﴿67﴾
مُسْتَكْبِرِينَ بِهِۦ سَٰمِراً تُهْجِرُونَ ﴿68﴾ أَفَلَمْ يَدَّبَّرُوا الْقَوْلَ أَمْ جَآءَهُم
مَّا لَمْ يَأْتِ ءَابَآءَهُمُ الْأَوَّلِينَ ﴿69﴾ أَمْ لَمْ يَعْرِفُوا رَسُولَهُمْ فَهُمْ لَهُۥ
مُنكِرُونَ ﴿70﴾ أَمْ يَقُولُونَ بِهِۦ جِنَّةٌ بَلْ جَآءَهُم بِالْحَقِّ
وَأَكْثَرُهُمْ لِلْحَقِّ كَٰرِهُونَ ﴿71﴾ وَلَوِ اتَّبَعَ الْحَقُّ أَهْوَآءَهُمْ لَفَسَدَتِ
السَّمَٰوَٰتُ وَالْأَرْضُ وَمَن فِيهِنَّ بَلْ أَتَيْنَٰهُم بِذِكْرِهِمْ فَهُمْ عَن
ذِكْرِهِم مُّعْرِضُونَ ﴿72﴾ أَمْ تَسْـَٔلُهُمْ خَرْجاً فَخَرَاجُ رَبِّكَ خَيْرٌ
وَهُوَ خَيْرُ الرَّٰزِقِينَ ﴿73﴾ وَإِنَّكَ لَتَدْعُوهُمُ إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿74﴾
وَإِنَّ الَّذِينَ لَا يُومِنُونَ بِالْآخِرَةِ عَنِ الصِّرَٰطِ لَنَٰكِبُونَ ﴿75﴾

61. Da waɗanda suke bada abinda suka bayar (na sadaka ko kyauta ko aiki nagari,) alhali zukatansu tana fargaba, (kada ya zama ba a karɓa daga garesu ba,) saboda su masu komawa ne izuwa Ubangijinsu.
62. To, waɗannan sune masu garaje a cikın alheri, sune marigaya garta (a cikin sanin Allah Maɗaukakin Sarki).
63. Barna kallafa wa kowa sai ikonsa, (wanda bai sami ikon salla a tsaye ba yayi a zaune, wanda bai same ikon yayi azumi baya buda baki,) littafi mai firici da gaskiya yana garemu (shine LAUHUL MAHFUZU, an rubuta dukkan ayyuka a cikinsa,su waɗannan muminai) masu wannan aiki baza a zalunccsu (komai) ba, (ta rage ladan aiki ko ƙari kan mummunan aiki).

(KAFIRAI DA AYYUKANSU DA SABUBBAN AIKIN)

64. Bari! Zukatan kafirai suna cikin magagi daga wannan (Alƙur'ani,) kuma suna da ayyuka komabayan wannan (abin ambato ga muminai,) su ɗasuke aikata ta, za ayi musu azaba a kanta).
65. Har lokacin da muka kama manya-manyansu da azaba, sai gasu suna kururuwa , (shine ranar Badar).
66. To, kada kuyi kururuwa yau, haƙiƙa ku baza a hana muku azabadaga garemu ba.
67. Haƙiƙa ayoyina (na ƙur'ani) sun kasance ana karanta su a gareku, kuka zama kuna girkawa aguje dabaya-dabaya a kan duga duganku.
68. Kuna masu ƙemaimai ga barin imani a dakin Allah Maɗaukakin Sarki, da humminsa wato Makka, halin ƙasancewarku ƙungiya masu (aljama wato hira da dare daura da dakin Allah Maɗaukakin Sarki, kuna surutan banza a cikin Annabi Sallallahu alaihi wasallama da Alƙur'anil-Karim.
69. Shin basu dubada kyau bane a cikin fahimtar maganar Alƙur'ani, me shiryarwa bisa gaskiyar sa (Sallallahu alaihi wasallama) ko kuwa abinda bai zowa iyayensu na farko bane yazo musu?
70. Ko basu san manzon nasu ba ne, su suna musunsa?
71. Ko kuma suna cewa akwai motsuwar hankali a gareshi, kai shi dai yazo musu da gaskiya ne (Alƙur'ani wanda ya tattara a kan tauhidi da shari'o'in Musulunci). Yawaicinsu masu kin gaskiya ne.
72. Da alƙur'an zai bi son soye-soyen zukatansu, (shine yazo musu da abinda yake dacewa da son zuciyarsu na daga sharikai da dangana da ga Allah, Allah ya girma ga barin wannan) da sammai da ƙassai sun rushe, da wanda yakc cikinsu (saboda. samuwar tataɓurza, a tsakanin su mahukuntan dangane da al'ada in suka ƙirgu,) Kai! Mun zo musune da ɗaukakarsu (wato Alƙur'ani, wanda ambaton su yake cikinsa). Su masu bijirewa ne ga barin ambaton nan nasu.
73. Ko ka tambaye su lada ne (a bisa abinda ka zo musu dashine na daga imani,) to ladan Ubangijinka shine yafi amfani, to, Ubangiji shine mafificin masu azurtawa.
74. Haƙiƙa kai kana kiran sune izuwa tafarki madaidaici (DiniIIslami).
75. Haƙiƙa waɗanda basu bada gaskiya da ranar Lahira ba, masu karkacewa ne ga barin hanyar gaskiya

ربع

* وَلَوْ رَحِمْنَٰهُمْ وَكَشَفْنَا مَا بِهِم مِّن ضُرٍّ لَّلَجُّواْ فِي طُغْيَٰنِهِمْ يَعْمَهُونَ ﴿76﴾
وَلَقَدْ أَخَذْنَٰهُم بِالْعَذَابِ فَمَا اَسْتَكَانُواْ لِرَبِّهِمْ وَمَا يَتَضَرَّعُونَ ﴿77﴾
حَتَّىٰٓ إِذَا فَتَحْنَا عَلَيْهِم بَابًا ذَا عَذَابٍ شَدِيدٍ إِذَا هُمْ
فِيهِ مُبْلِسُونَ ﴿78﴾ وَهْوَ الَّذِيٓ أَنشَأَ لَكُمُ السَّمْعَ وَالْأَبْصَٰرَ
وَالْأَفْـِٔدَةَ قَلِيلًا مَّا تَشْكُرُونَ ﴿79﴾ وَهْوَ الَّذِي ذَرَأَكُمْ فِي الْأَرْضِ
وَإِلَيْهِ تُحْشَرُونَ ﴿80﴾ وَهْوَ الَّذِي يُحْيِۦ وَيُمِيتُ وَلَهُ اخْتِلَٰفُ
الَّيْلِ وَالنَّهَارِ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿81﴾ بَلْ قَالُواْ مِثْلَ مَا قَالَ الْأَوَّلُونَ ﴿82﴾
قَالُوٓاْ أَٰذَا مِتْنَا وَكُنَّا تُرَابًا وَعِظَٰمًا إِنَّا لَمَبْعُوثُونَ ﴿83﴾
لَقَدْ وُعِدْنَا نَحْنُ وَءَابَآؤُنَا هَٰذَا مِن قَبْلُ إِنْ هَٰذَا
إِلَّآ أَسَٰطِيرُ الْأَوَّلِينَ ﴿84﴾ قُل لِّمَنِ الْأَرْضُ وَمَن فِيهَا إِن كُنتُمْ
تَعْلَمُونَ ﴿85﴾ سَيَقُولُونَ لِلَّهِ قُلْ أَفَلَا تَذَّكَّرُونَ ﴿86﴾
قُلْ مَن رَّبُّ السَّمَٰوَٰتِ السَّبْعِ وَرَبُّ الْعَرْشِ
الْعَظِيمِ ﴿87﴾ سَيَقُولُونَ لِلَّهِ قُلْ أَفَلَا تَتَّقُونَ ﴿88﴾ قُلْ مَنۢ
بِيَدِهِۦ مَلَكُوتُ كُلِّ شَيْءٍ وَهْوَ يُجِيرُ وَلَا يُجَارُ عَلَيْهِ إِن كُنتُمْ
تَعْلَمُونَ ﴿89﴾ سَيَقُولُونَ لِلَّهِ قُلْ فَأَنَّىٰ تُسْحَرُونَ ﴿90﴾

(TAURIN KANSU A KAN SHIRKA TAREDA BAYYANAR DALILAI)

76. Da Mun jiƙansu mun yaye musu abinda yake garesu na daga tsanani, (wato yunwa data samesu a Makka shekara bakwai,) dasun zarce suna dirilicewa a cikin shisshiginsu.
77. Haƙiƙa Mun riƙe su da azaba (yunwa,) basu tawalu'u ga Ubangijinsu ba, kuma basu ƙanƙan dakai izuwa Allah (da roƙonsa) ba
78. Har a yayin da muka buɗe musu kofa ma'abuciyar azaba mai tsanani (shine kisa ranar Badar) sai gasu suna debewa hasu daga dukkan alheri (a wannan ranar.)
79. Shine wanda ya halicci kunnuwa a garekuda idanduna da zukata. Kaɗan ne ƙwarai kuke godewa Allah.
80. Kuma shine ya halicce ku a cikin ƙasa izuwa gareshi kuke komawa.
81. Shine wanda yake rayawa (da busa rai a cikin tsoka), yake kashewa, kaikawon dare da rana na Allah ne ta wajen kari ko tawaya, Shin ba kwayi hankali ba, ku lura da aikin Allah.
82. Kai! bari sun faɗi irin yadda mutanen farko suka faɗa,
83. Shine sukace shin yanzu idan mun mutu mun zama turɓaya da ƙasusuwa, yanzu haƙiƙa muza a tashe mu?
84. Haƙiƙa an alƙawarta mana wannan tashi bayan mutuwarmu, da iyayenmu tun gaba, wannan bai kasance ba sai ƙaryace-ƙaryacen mutanen farko.
85. Cene (dasu) ƙasa da wanda yake cikin ta na waye, in kun kasance kun san (mana llakin ta)
86. Da sannu zasu ce, "Na Allah ne", Cene (dasu) "Shin ba kwa wa'azantu ba (ku sani cewa mai iko bisa halitta da farko mai iko ne bisa rayawa bayan mutuwa?")
87. Cene, "Wanene Ubangijin sammai bakwai, wanene Ubangijin Al'arshi mai girma?"
88. Zasu ce na Allah ne, Cene, "Shin ba kwa tsoraci (bautar waninsa) ba".
89. Cene, "Wanene zuzzurfan mulkin kome yake cikin ikonsa, shine mai kiyayewa ba a kiyaye shi, in kun kasance kun san (mahaliccin ta?")
90. Zasu ce "Na Allah ne", cene, "To, donme ake yaudararku (kuke juyawa ga barin gaskiya wato bautawa Allah shi kaɗai".)

بَلْ أَتَيْنَٰهُم بِالْحَقِّ وَإِنَّهُمْ لَكَٰذِبُونَ ﴿91﴾ مَا اتَّخَذَ اللَّهُ مِن وَلَدٍ
وَمَا كَانَ مَعَهُۥ مِنْ إِلَٰهٍ إِذًا لَّذَهَبَ كُلُّ إِلَٰهٍ بِمَا خَلَقَ وَلَعَلَا بَعْضُهُمْ
عَلَىٰ بَعْضٍ سُبْحَٰنَ اللَّهِ عَمَّا يَصِفُونَ ﴿92﴾ عَٰلِمُ الْغَيْبِ
وَالشَّهَٰدَةِ فَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿93﴾ قُل رَّبِّ إِمَّا تُرِيَنِّي
مَا يُوعَدُونَ ﴿94﴾ رَبِّ فَلَا تَجْعَلْنِي فِي الْقَوْمِ الظَّٰلِمِينَ ﴿95﴾
وَإِنَّا عَلَىٰ أَن نُّرِيَكَ مَا نَعِدُهُمْ لَقَٰدِرُونَ ﴿96﴾ إِدْفَعْ بِالَّتِي هِيَ
أَحْسَنُ السَّيِّئَةَ نَحْنُ أَعْلَمُ بِمَا يَصِفُونَ ﴿97﴾ * وَقُل رَّبِّ أَعُوذُ بِكَ
مِنْ هَمَزَٰتِ الشَّيَٰطِينِ ﴿98﴾ وَأَعُوذُ بِكَ رَبِّ أَنْ يَحْضُرُونِ ﴿99﴾
حَتَّىٰ إِذَا جَا أَحَدَهُمُ الْمَوْتُ قَالَ رَبِّ ارْجِعُونِ ﴿100﴾
لَعَلِّي أَعْمَلُ صَٰلِحًا فِيمَا تَرَكْتُ كَلَّا إِنَّهَا كَلِمَةٌ هُوَ قَآئِلُهَا
وَمِن وَرَآئِهِم بَرْزَخٌ إِلَىٰ يَوْمِ يُبْعَثُونَ ﴿101﴾ فَإِذَا نُفِخَ فِي الصُّورِ
فَلَا أَنسَابَ بَيْنَهُمْ يَوْمَئِذٍ وَلَا يَتَسَآءَلُونَ ﴿102﴾ فَمَن ثَقُلَتْ
مَوَٰزِينُهُۥ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ الْمُفْلِحُونَ ﴿103﴾ وَمَنْ خَفَّتْ
مَوَٰزِينُهُۥ فَأُوْلَٰٓئِكَ الَّذِينَ خَسِرُوا أَنفُسَهُمْ فِي جَهَنَّمَ خَٰلِدُونَ ﴿104﴾
تَلْفَحُ وُجُوهَهُمُ النَّارُ وَهُمْ فِيهَا كَٰلِحُونَ ﴿105﴾

ثمن

91. Kai mun zo musu da gaskiya ne, haƙiƙa su maƙaryata ne.

(ALLAH BASHI DA DA)

92. Ubangiji bai riƙi da ba, bashi da wani abin bautawa tare dashi, to, yayin nan da akwai wani ubangiji tare dashi, da kowane ubangijin saiya tafi da abinda ya halitta, (ya hana ɗan uwansa burunƙasa a kanta,) da kuma sashinsu ya rinjayi sashi, (kamar yadda sarakunan duniya suke yi,) Tsarki ya tabbatar wa Ubangiji ga barin abinda suke kwatantawa.

(FUSKANTARWAR UBANGIJI GA ANNABINSA SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

93. Masanin asirin fake dana sarari, Ya girmama ga barin abinda suke shirkanta shi tare dashi.
94. Cene, "Ubangiji in ka nuna min abinda ake musu gargaɗi (na azaba),
95. To kadaka sa ni a cikin mutane azzalumai (don kada in halaka da halakarsu").
96. Haƙiƙa mu masu iko ne bisa mu nuna maka abinda muke musu alƙawari dashi,
97. Ije mummuna da tada datafi kyau. (wannan gaban umarni dayaki ne,) Mune masana da abinda suke sufantawa (na ƙarya, zamuyi musu sakamako a kansa).
98. Cene, "Ubangiji ina neman tsaruwa dakai daga zungure-zunguren nan na shaiɗanu,
99. "Ina neman tsaruwa dakai Ubangiji a kan su halarto ni (a cikin al'amurana, saboda su basa halartowa saida cuta".)
100. Har a yayin da mutuwa ta zowa ɗayansu, (yaga mazauninsa na wutadana aljanna daya bada gaskiya,) sai yace, Ya Ubangijina ku komo da ni
101. Saboda ƙaunar na aikata nagari, (wato in kaɗaita Allah,) ya kasance ya zama a cikin abinda na tozarta (na daga raina, sai Ubangiji yace,) Kai, bazaka koma ba, haƙiƙa ita wannan kalma (ta Allah ka maido da ni,) kalma ce dashine mafaɗinta (batada fa'ida,) akwai shamaki a gabansu (mai hana su komowa duniya,) harizuwa ranar daza a tashesu, (wanda babu komowa bayansa).
102. To, idan akayi busa a cikin ƙaho (busa ta farko,) to, babu dangance-dangance a tsakaninsu a wannan rana (dasuke alfahari da ita,) bakuma zasu tambayi junansu (gareta) ba. (Saboda abindazai gigita su na daga lamarin alƙiyama, ko da yake suna farkawa a wani lokacin wanda ayar FA AKBALA BA ALUHUM ALA BA ALIN ta nuna.
103. To wanda ma'aunansa sukayi nauyi (da aiki nagari,) to, wancananka sune haƙiƙa nin marabauta.
104. Wanda ma'aunansa sukayi shafal (da miyagun ayyuka,) to, waɗancananka sune waɗanda suka taɓar da kawunansu, to, su, madawwama ne cikin jahannama.
105. Wuta tana toye fuskokinsu, su masu gayau da haƙorane a cikinta.

أَلَمْ تَكُنْ ءَايَٰتِي تُتْلَىٰ عَلَيْكُمْ فَكُنتُم بِهَا تُكَذِّبُونَ ﴿106﴾
قَالُواْ رَبَّنَا غَلَبَتْ عَلَيْنَا شِقْوَتُنَا وَكُنَّا قَوْماً ضَآلِّينَ ﴿107﴾
رَبَّنَا أَخْرِجْنَا مِنْهَا فَإِنْ عُدْنَا فَإِنَّا ظَٰلِمُونَ ﴿108﴾
قَالَ اخْسَئُواْ فِيهَا وَلَا تُكَلِّمُونِ ﴿109﴾ إِنَّهُۥ كَانَ فَرِيقٌ
مِّنْ عِبَادِي يَقُولُونَ رَبَّنَا ءَامَنَّا فَاغْفِرْ لَنَا وَارْحَمْنَا وَأَنتَ
خَيْرُ الرَّٰحِمِينَ ﴿110﴾ فَاتَّخَذتُّمُوهُمْ سُخْرِيّاً حَتَّىٰ أَنسَوْكُمْ ذِكْرِي
وَكُنتُم مِّنْهُمْ تَضْحَكُونَ ﴿111﴾ إِنِّيَ جَزَيْتُهُمُ الْيَوْمَ بِمَا صَبَرُواْ أَنَّهُمْ
هُمُ الْفَآئِزُونَ ﴿112﴾ قَالَ كَمْ لَبِثْتُمْ فِي الْأَرْضِ عَدَدَ سِنِينَ ﴿113﴾
قَالُواْ لَبِثْنَا يَوْماً أَوْ بَعْضَ يَوْمٍ فَسْئَلِ الْعَآدِّينَ ﴿114﴾
قَالَ إِن لَّبِثْتُمْ إِلَّا قَلِيلاً لَّوْ أَنَّكُمْ كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿115﴾
* أَفَحَسِبْتُمْ أَنَّمَا خَلَقْنَٰكُمْ عَبَثاً وَأَنَّكُمْ إِلَيْنَا لَا تَرْجِعُونَ ﴿116﴾
فَتَعَٰلَى اللَّهُ الْمَلِكُ الْحَقُّ لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ رَبُّ الْعَرْشِ الْكَرِيمِ ﴿117﴾
وَمَن يَدْعُ مَعَ اللَّهِ إِلَٰهاً ءَاخَرَ لَا بُرْهَٰنَ لَهُۥ بِهِۦ
فَإِنَّمَا حِسَابُهُۥ عِندَ رَبِّهِۦ إِنَّهُۥ لَا يُفْلِحُ الْكَٰفِرُونَ ﴿118﴾
وَقُل رَّبِّ اغْفِرْ وَارْحَمْ وَأَنتَ خَيْرُ الرَّٰحِمِينَ ﴿119﴾

ربع

106. Shin ayoyina basu kasance ana karanta su bane gareku kuka zamo kuna ƙaryatawa da ita?
107. Sukace, Ya Ubangijinmu, tsiy-armu ce tayi rinjaye kanmu, muka kasance mutane batattu.
108. Ya Ubangijinmu fitar da mu daga cikinta, idan mun koma izuwa sabonka to haƙiƙa mu masu zaluntar kanmu ne.
109. Sai Ubangiji yace (dasu da harshen Mala'iku bayan gwargwadon duniya sau biyu,) As! A cikin ta, kadaku ,kuma magana dani, (To, saisu debe kauna daga rahamar Allah).
110. Haƙiƙa al'amarin akwai wađansu jama'a na daga bayina Muhajirai na Sahabban Annabi Sallallahu alaihi wasallama, suna cewa Ya Ubangijinmu, mun bada gaskiya kayi gafara garemu, ka jiƙanmu, Kaine fiyayyen masu jinƙai.
111. Sai kuka riƙe su sosai (kamar Bilalu dasuhaibu da Ammaru da Salmanu, Allah ya ƙara yarda a garesu) har suka mantar daku ,ambatona (kuka bar shi saboda kun shagala da izgili dasu.) Kun kasance kuna yin dariya daga garesu.
112. "Ni nayi musu sakamako a yau (saboda haƙurinsu, haƙiƙa su, sune marabauta)".
113. Sai Ubangiji yace (dasu da harshen maliku mataskacin wuta,) "Nawa kuka zauna (a ƙasa wato cikin duniya da ƙaburburanku na adadin shekam?"
114. Sukace, "Mun zauna wuni ko sashin wuni, (sun yi kokonto cikin wannan, sun ga gajartarsa saboda girman abinda suke ciki na azaba,) tambayi masu ƙirgawa".
115. Sai Ubangiji ya fađa (da harshen Mala'iku) "Baku zauna ba sai kađan da kun kasance kun san (gwargwadon zamanku na daga tsawon zama đaya, zama kađan dangane da zamanku na cikin wuta).
116. Shin kuna zaton mun halicce kune don wasa? Kuma cewa ko baza a komo daku ,zuwa garemu ba.
117. Sarki Allah ya tsarkaka (ga barin wasa), Sarki matabbaci, babu abin bautawa da gaskiya sai Shi, Ubangijin Al'arshi mai girma.
118. Duk wanda ya bautawa wanin Ubangiji daban tareda Allah da ba hujja a gareshi (ta bauta masa,) to, haƙiƙa dai sakama-konsu yana wajen Ubangijinsa, haƙiƙa shi al'amarin kafirai bazasu tsira ba.
119. Cene, "Ubangijina kayi mana gafara, ka jiƙanmu, kaine fiyayyen masu jinƙai".

24 سُورَةُ النُّورِ مَدَنِيَّةٌ

وَهِيَ ثِنْتَانِ وَسِتُّونَ ءَايَةً 62

بِسْمِ اِ۬للَّهِ اِ۬لرَّحْمَٰنِ اِ۬لرَّحِيمِ

سُورَةٌ أَنزَلْنَٰهَا وَفَرَضْنَٰهَا وَأَنزَلْنَا فِيهَا ءَايَٰتِۭ بَيِّنَٰتٍ لَّعَلَّكُمْ تَذَّكَّرُونَ ﴿1﴾ اَ۬لزَّانِيَةُ
وَالزَّانِے فَاجْلِدُواْ كُلَّ وَاحِدٍ مِّنْهُمَا مِاْئَةَ جَلْدَةٍ وَلَا تَأْخُذْكُم بِهِمَا رَأْفَةٌ فِے دِينِ اِ۬للَّهِ
إِن كُنتُمْ تُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ وَالْيَوْمِ اِ۬لْءَاخِرِ وَلْيَشْهَدْ عَذَابَهُمَا طَآئِفَةٌ مِّنَ اَ۬لْمُؤْمِنِينَ ﴿2﴾
اَ۬لزَّانِے لَا يَنكِحُ إِلَّا زَانِيَةً أَوْ مُشْرِكَةً وَالزَّانِيَةُ لَا يَنكِحُهَا إِلَّا زَانٍ أَوْ مُشْرِكٌ
وَحُرِّمَ ذَٰلِكَ عَلَى اَ۬لْمُؤْمِنِينَ ﴿3﴾ وَالَّذِينَ يَرْمُونَ اَ۬لْمُحْصَنَٰتِ ثُمَّ لَمْ يَأْتُواْ بِأَرْبَعَةِ
شُهَدَآءَ فَاجْلِدُوهُمْ ثَمَٰنِينَ جَلْدَةً وَلَا تَقْبَلُواْ لَهُمْ شَهَٰدَةً أَبَدًا وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ
اُ۬لْفَٰسِقُونَ ﴿4﴾ إِلَّا اَ۬لَّذِينَ تَابُواْ مِنۢ بَعْدِ ذَٰلِكَ وَأَصْلَحُواْ فَإِنَّ اَ۬للَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿5﴾
وَالَّذِينَ يَرْمُونَ أَزْوَٰجَهُمْ وَلَمْ يَكُن لَّهُمْ شُهَدَآءُ إِلَّا أَنفُسُهُمْ فَشَهَٰدَةُ أَحَدِهِمْ
أَرْبَعَ شَهَٰدَٰتٍ بِاللَّهِ إِنَّهُۥ لَمِنَ اَ۬لصَّٰدِقِينَ ﴿6﴾ وَالْخَٰمِسَةُ أَنْ لَّعْنَتُ اُ۬للَّهِ عَلَيْهِ
إِن كَانَ مِنَ اَ۬لْكَٰذِبِينَ ﴿7﴾ وَيَدْرَؤُاْ عَنْهَا اُ۬لْعَذَابَ أَن تَشْهَدَ أَرْبَعَ شَهَٰدَٰتٍ
بِاللَّهِ إِنَّهُۥ لَمِنَ اَ۬لْكَٰذِبِينَ ﴿8﴾ وَالْخَٰمِسَةُ أَنْ غَضِبَ اَ۬للَّهُ عَلَيْهَا إِن كَانَ مِنَ
اَ۬لصَّٰدِقِينَ ﴿9﴾ وَلَوْلَا فَضْلُ اُ۬للَّهِ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَتُهُۥ وَأَنَّ اَ۬للَّهَ تَوَّابٌ حَكِيمٌ ﴿10﴾

Suratun Nuri

A Madina Aka. Saukar Da Ita Ayoyinta Sittin Da Biyu. (62)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

(WANNAN SURA TA TARA HUKUNCE-HUKUNCE DA LADABAI NA MUSULUMCI WACCE TAKE KIYAYE DANGANTAKAR AL'UMMA DA MUTUNCINSU) KIRARI DAGA ALLAH GA WANNAN SURA

1. Wannan sura ce muka saukar da ita, Muka wajabta abinda yake cikinta (na daga hukunce-hukunce,) Muka saukar da ayoyi mabayyanan (ma'anoni) a cikinta don a wa'azantu. (ZINA DA HADDIN TA)
2. Mazinaciya da mazinaci (waɗanda bakatangantattu ba, saboda jefe su sunna Tace ayi,) to, kudoki kowane daya daga cikinsu bulala ɗari, (kuma sunnar Annabi Alaihissalam ta ƙara.Baƙuntarwa shekara guda, magudanci wato bawa kuma bisa rabin abinda aka ambata. Kada tausayinsu ya riƙe ku, a cikin addinin Allah, (harkubar wani abuna daga haddinsu) in kun kasance kun bada gaskiya da Allah da ranar Lahira, jama'a na muminai su halarci bulalar tasu.
3. Mazinaci baya aure sai mazinaciyako mushurika, mazinaciyabata aure sai mazinaci ko mushiriki, an haramta auren mazinata ga muminai (wato karuwa i, wannan ya sauka ne lokacin da fuƙara'u na mahajirai suka nemi su auri karuwa i na mushirikai, alhali an ribato su donsu dinga ciyar dasu, amma an shafe wannan aya da faɗin Ubangiji:Kuauri zawarawa na daga gareku).

(ƘAZAF DA HADDINSA)

4. Waɗannan dasuke yi wa mataye kamammu kazaf, sannan basu zoda shedu hudu ba (masu shaidawa sun gansu suna zina), to ku doki kowane ɗaya daga cikinsu bulala tamanin, kadaku ,karɓi shaidarsu (a cikin komai) har abada, wadancananka sune fasikai (Don sun , aikata kabira).
5. Sai waɗanda suka tuba bayan wancananka sukayi kyakkyawan aiki, to, haƙiƙa Ubangiji mai gafara ne (garesu) mai jinƙai (daya kimsa musu tuba, to, sai a karɓi shaidarsu).

(KAZAF DIN MIJI GA MATA TASA)

6. Waɗannan da sukayi wa matayensu kazaf kuma basu da shaidu a kansa sai kansu, (wancananka ya afku ga waɗansu jama'a na daga sahabbai,) to, shaidar ɗayansu shaidu ne guda hudu, (wato) ya rantse da Allah haƙiƙa shi yana daga cikin magasgata (a cikin abinda ya jefi. mata tasa dashi).
7. Rantsuwa ta biyar cewa la'anar Allah tana gareshi inya kasance daga cikin maƙaryata.
8. Yana ije haddin zina ga buran ta, ta rantse rantsuwa guda hudu da Ubangiji haƙiƙa shi mijin nan nata yana cikin maƙaryata (cikin ƙazafin dayayi mata).
9. Rantsuwa ta biyar cewa fushin Allah na kanta in ya kasance cikin masu gaskiya.
10. Ba don falalar Allah garekuda jiƙansa ba (dayayi muku sittira a cikin wannan, daya gaggauta ukuba a gareku,) haƙiƙa Ubangiji mai yawan karɓar tuba ne, gwani (cikin abinda yayi hukunci dashi.)

ثمن

* إِنَّ ٱلَّذِينَ جَآءُو بِٱلْإِفْكِ عُصْبَةٞ مِّنكُمْۖ لَا تَحْسِبُوهُ شَرّٗا لَّكُمۖ بَلْ هُوَ
خَيْرٞ لَّكُمْۖ لِكُلِّ ٱمْرِيٕٖ مِّنْهُم مَّا ٱكْتَسَبَ مِنَ ٱلْإِثْمِۖ وَٱلذِے تَوَلّ۪يٰ
كِبْرَهُۥ مِنْهُمْ لَهُۥ عَذَابٌ عَظِيمٞۖ 11 لَّوْلَآ إِذْ سَمِعْتُمُوهُ ظَنَّ ٱلْمُؤْمِنُونَ
وَٱلْمُؤْمِنَٰتُ بِأَنفُسِهِمْ خَيْراٗ وَقَالُواْ هَٰذَآ إِفْكٞ مُّبِينٞۖ 12 لَّوْلَا جَآءُو
عَلَيْهِ بِأَرْبَعَةِ شُهَدَآءَۖ فَإِذْ لَمْ يَاتُواْ بِٱلشُّهَدَآءِ فَأُوْلَٰٓئِكَ عِندَ ٱللَّهِ
هُمُ ٱلْكَٰذِبُونَۖ 13 وَلَوْلَا فَضْلُ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَتُهُۥ
فِے ٱلدُّنْي۪ا وَٱلْءَاخِرَةِ لَمَسَّكُمْ فِے مَآ أَفَضْتُمْ فِيهِ عَذَابٌ عَظِيمٌ 14
إِذْ تَلَقَّوْنَهُۥ بِأَلْسِنَتِكُمْ وَتَقُولُونَ بِأَفْوَاهِكُم مَّا لَيْسَ لَكُم بِهِۦ عِلْمٞ وَتَحْسِبُونَهُۥ
هَيِّناٗ وَهُوَ عِندَ ٱللَّهِ عَظِيمٞۖ 15 وَلَوْلَآ إِذْ سَمِعْتُمُوهُ قُلْتُم مَّا يَكُونُ
لَنَآ أَن نَّتَكَلَّمَ بِهَٰذَا سُبْحَٰنَكَ هَٰذَا بُهْتَٰنٌ عَظِيمٞۖ 16 يَعِظُكُمُ
ٱللَّهُ أَن تَعُودُواْ لِمِثْلِهِۦٓ أَبَداً إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَۖ 17 وَيُبَيِّنُ ٱللَّهُ
لَكُمُ ٱلْءَايَٰتِۖ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌۖ 18 إِنَّ ٱلَّذِينَ يُحِبُّونَ
أَن تَشِيعَ ٱلْفَٰحِشَةُ فِے ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٞ فِے ٱلدُّنْي۪ا
وَٱلْءَاخِرَةِۖ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ وَأَنتُمْ لَا تَعْلَمُونَۖ 19 وَلَوْلَا فَضْلُ
ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَتُهُۥ وَأَنَّ ٱللَّهَ رَءُوفٞ رَّحِيمٞۖ 20

11. Haƙiƙa waɗannan da suka zoda kuta karya (ga Nana A'isha Allah ya ƙara yarda a gareta,) jama'a ne daga cikinku (mumi-nai, wato Hassanu Ibn Sabitin da Abdullahi Ibn Ubaiyin, da Misɗahu da Haruna tu binti Jahashin,) kadaku ,zaci wannan kuce (wato gunɗumemiyar ƙarya) sharrine a gareku, bari! Shi dai alheri ne gareku, (Allah zai baku lada saboda shi Allah kuma zai bayyana kuɓutar Nana A'isha Allah ya ƙara yarda a gareta, to, ƙissar kuma sananniyace.) Abinda kowane daga cikinsu ya tsuwurwurta na zunubi ya tabbata gareshi, wanda yajibinci gunɗimemansa daga cikinsu, (wato ya fara kutsawa ciki ya daidaita shi wato Abdullahi Ibn Ubaiyu,) azaba gunɗimemiya ta tabbata gareshi (ranar alƙiyama Itace wuta).
12. Donme zamanin da kukaji shi, muminai maza da mata basuyi zaton alheri ga kawukansu ba, suce, "Wannan girbe ne mabayyani".
13. Donme basu zoda shaidu guda hudu a kai ba, to, tunda basu zoda shaidu hudu ba, haƙiƙa waɗancananka gurin Ubangiji sune ainihin maƙaryata.
14. Ba don falalar Allah gareku a duniya da lahira ba, da azaba mai girma ta shafe ku cikin abinda kuka kutsa a cikinsa (ranar lahira).
15. Zamanin da kuke curo shi da harasanku, kuna faɗa da bakunanku abinda bakuda ilimi dashi kuna zaton sa sassauka, alhali shi kuwa mai girma ne wurin Ubangiji, (hakin daka raina shi yake tsoka ne ido).
16. Donme zamanin da kukaji shi baku ce "Bazai kamatamu yi furici da wannan ba. Tsarki ya tabbatar maka, wannan ƙaryace mai girma".
17. Allah yanayi muku gargaɗi daga ku koma ga irin wannan har abada in kun kasance muminai.
18. Allah yana yi muku bayanin ayoyinsa (a cikin umarni da hani,) Allah masanine (da abinda yake umarninku dashi ko yake hani ga buransa) gwanine (cikinsa).
19. Haƙiƙa waɗannan dake kaunar mugunyar magana ta daidaita a cikin waɗanda suka bada gaskiya, (ta wajen dangana ta izuwa garesu, wato sune wancananka ƙungiya). Azaba mai radadi ta tabbata garesu duniya da lahira, (a dunuya da haddin kazaf, lahira dashiga wuta,)Allah yasan (kuɓutar Nana A'isha Allah ya ƙara yarda a gareta, tafita sumul, alhali) ku kuwa baku sani ba.
20. Ba don falalar Allah gareku ba (da jinkansa da cewa kuma Ubangiji mai Jinƙai ne) da rahama (da ku,) kuma cewa haƙiƙa Ubangiji mai yawan rahama ne (da ku, dayayi gaggawar kama kuda uƙuba.)

حزب

۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّبِعُواْ خُطُوَٰتِ ٱلشَّيْطَٰنِۚ وَمَن يَتَّبِعْ خُطُوَٰتِ
ٱلشَّيْطَٰنِ فَإِنَّهُۥ يَأْمُرُ بِٱلْفَحْشَآءِ وَٱلْمُنكَرِۚ وَلَوْلَا فَضْلُ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ
وَرَحْمَتُهُۥ مَا زَكَىٰ مِنكُم مِّنْ أَحَدٍ أَبَدًا وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يُزَكِّي
مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿٢١﴾ وَلَا يَأْتَلِ أُوْلُواْ ٱلْفَضْلِ مِنكُمْ
وَٱلسَّعَةِ أَن يُؤْتُوٓاْ أُوْلِي ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْمَسَٰكِينَ وَٱلْمُهَٰجِرِينَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ
وَلْيَعْفُواْ وَلْيَصْفَحُوٓاْۗ أَلَا تُحِبُّونَ أَن يَغْفِرَ ٱللَّهُ لَكُمْۚ وَٱللَّهُ
غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٢٢﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَرْمُونَ ٱلْمُحْصَنَٰتِ ٱلْغَٰفِلَٰتِ ٱلْمُؤْمِنَٰتِ
لُعِنُواْ فِي ٱلدُّنْيَا وَٱلْأٓخِرَةِ وَلَهُمْ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿٢٣﴾ يَوْمَ تَشْهَدُ عَلَيْهِمْ
أَلْسِنَتُهُمْ وَأَيْدِيهِمْ وَأَرْجُلُهُم بِمَا كَانُواْ يَعْمَلُونَ ﴿٢٤﴾
يَوْمَئِذٍ يُوَفِّيهِمُ ٱللَّهُ دِينَهُمُ ٱلْحَقَّ وَيَعْلَمُونَ أَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْحَقُّ ٱلْمُبِينُ ﴿٢٥﴾
ٱلْخَبِيثَٰتُ لِلْخَبِيثِينَ وَٱلْخَبِيثُونَ لِلْخَبِيثَٰتِۖ وَٱلطَّيِّبَٰتُ لِلطَّيِّبِينَ
وَٱلطَّيِّبُونَ لِلطَّيِّبَٰتِۚ أُوْلَٰٓئِكَ مُبَرَّءُونَ مِمَّا يَقُولُونَۖ
لَهُم مَّغْفِرَةٌ وَرِزْقٌ كَرِيمٌ ﴿٢٦﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
لَا تَدْخُلُواْ بُيُوتًا غَيْرَ بُيُوتِكُمْ حَتَّىٰ تَسْتَأْنِسُواْ وَتُسَلِّمُواْ عَلَىٰٓ
أَهْلِهَاۚ ذَٰلِكُمْ خَيْرٌ لَّكُمْ لَعَلَّكُمْ تَذَكَّرُونَ ﴿٢٧﴾

21. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya, kadaku ,bi ƙawace-ƙawacen shaiɗan, wanda yabi ƙawace-ƙawacen shaiɗan haƙiƙa shi shaiɗan yana umarni da alfasha da mummunan aiki a shari'a.Badon falalar Allah gare kuda rahama tasa badaya daga cikinkuda bazai tsarkaka har abada, amma Allah yana tsarkake wanda yaga dama (daga zunibi da karɓar tubansa,) Allah mai ji ne (ga abinda kuka faɗa), masanine (da abinda kuka nufa).

22. Kada ma'abuta falala (wato wadata) daga cikin kuda wadatasu rantse a kan baza suyi baiwa ga ma'abuta zumunci da miskinai, da muhajirai saboda Allah ba (ta sauka ne a cikin Sayyadina Abubakar Siddiƙu a kan bazai ciyar baga Musdahu gashi kuwa dan yakumbonsa ne wato dan khalatasa, miskini ne, muhajiri ne, dan Badar wato wanda ya halarci Badar ke nan, yayin daya afka a cikin kucen da akayi wa Nana A'isha Allah ya ƙara yarda a gareta, alhali kuwa da can shi yake ciyar dashi, yayin da waɗansu Sahabbai suka rantse a kan bazasu ciyar da duk wanda yayi zance da wani abu na daga kazaf ba) suyi rangwame suyi afuwa (garesu a cikin wancananka) Shin ba kwa son Allah yayi muku gafara ne? Allah mai ɗinbin gafara ne mai jinƙai (ga muminai, sai Sayyadina Abubakar Siddiƙu yace, A'a, ina so Allah yayi min gafara mana, yakoma ga Musdahu da abinda yake ciyarwa gareshi).

(ƘARSHEN ƘISSA)

23. Haƙiƙa waɗannan dasuke yin kazaf ga mataye kamammu da basu taɓa sanin yadda ake aikin alfasha ba, masu gasgatawa (da Allah da Manzonsa,) an tsine musu albarka duniya da lahira azabar rana mai girma na garesu.

24. Harsunansu za tayi shaida a kansu da hannayensu da ƙafafuwansu da abinda suka kasance suna aikatawa (na daga magana da aiki shine ranar Alƙiyama).

25. A wancananka rana ne Allah zai cika musu sakamakonsu na gaskiya, a ranan ne suke sanin haƙiƙa Ubangiji shine matabbacin Sarki mai bayyana ƙarya daga gaskiya, (Abdullahi ɗan Ubaiyu yana daga cikinsu).

26. Miyagun mataye da miyagun kalmomi sun tabbata ga miyagun mutane maza da mata, miyagun mutane sun tabbata ga miyagun mataye, daɗaɗan kalmomi da mataye sun tabbata ga dadadan mutane maza da mata, dadadan mazaje sun tabbata ga dadadan mataye, to wadancananka (daɗaɗan mazaje da mataye, waɗanda Nana A'isha da Safuwanu suna cikinsu, Allah ya ƙara yarda a garesu,) ababan kubutarwa ne daga abinda suke fadi (na kage,) gafarar Ubangiji na garesu da daɗaɗan mazaje da mataye da arziki mai girma (cikin aljanna, haƙiƙa Nana A'isha tayi alfahari da abubuwa yana daga cikin cewa an halicce ta daddaɗa, anyi mata alƙawarin gafara da arziki mai girma).

(NEMAN IZININ SHIGA GIDA DA LADABANSA)

27. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya! kadaku ,shiga dakuna da badakunanku ba har sai kun yi sallama kun nemi izini ga masu ita, (shine dayanku yace Assalamu alaikum, A'ad'hulu?' tamfar dayazo cikin Hadisi,) wancananku shi yafi alheri gareku, (na daga shiga bada neman izini ba) don ku wa'azantu.

فَإِن لَّمْ تَجِدُواْ فِيهَا أَحَداً فَلَا تَدْخُلُوهَا حَتَّىٰ يُؤْذَنَ لَكُمْ
وَإِن قِيلَ لَكُمُ ارْجِعُواْ فَارْجِعُواْ هُوَ أَزْكَىٰ لَكُمْ
وَاللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ عَلِيمٌ ﴿28﴾ لَّيْسَ عَلَيْكُمْ جُنَاحٌ أَن تَدْخُلُواْ بُيُوتاً
غَيْرَ مَسْكُونَةٍ فِيهَا مَتَاعٌ لَّكُمْ وَاللَّهُ يَعْلَمُ مَا تُبْدُونَ وَمَا تَكْتُمُونَ ﴿29﴾
ثمن * قُل لِّلْمُؤْمِنِينَ يَغُضُّواْ مِنْ أَبْصَارِهِمْ وَيَحْفَظُواْ فُرُوجَهُمْ
ذَٰلِكَ أَزْكَىٰ لَهُمْ إِنَّ اللَّهَ خَبِيرٌ بِمَا يَصْنَعُونَ ﴿30﴾
وَقُل لِّلْمُؤْمِنَاتِ يَغْضُضْنَ مِنْ أَبْصَارِهِنَّ وَيَحْفَظْنَ
فُرُوجَهُنَّ وَلَا يُبْدِينَ زِينَتَهُنَّ إِلَّا مَا ظَهَرَ مِنْهَا وَلْيَضْرِبْنَ بِخُمُرِهِنَّ
عَلَىٰ جُيُوبِهِنَّ وَلَا يُبْدِينَ زِينَتَهُنَّ إِلَّا لِبُعُولَتِهِنَّ أَوْ ءَابَآئِهِنَّ
أَوْ ءَابَآءِ بُعُولَتِهِنَّ أَوْ أَبْنَآئِهِنَّ أَوْ أَبْنَآءِ بُعُولَتِهِنَّ أَوْ إِخْوَانِهِنَّ
أَوْ بَنِيٓ إِخْوَانِهِنَّ أَوْ بَنِيٓ أَخَوَاتِهِنَّ أَوْ نِسَآئِهِنَّ أَوْ مَا مَلَكَتْ
أَيْمَانُهُنَّ أَوِ التَّٰبِعِينَ غَيْرِ أُوْلِي الْإِرْبَةِ مِنَ الرِّجَالِ
أَوِ الطِّفْلِ الَّذِينَ لَمْ يَظْهَرُواْ عَلَىٰ عَوْرَاتِ النِّسَآءِ وَلَا يَضْرِبْنَ
بِأَرْجُلِهِنَّ لِيُعْلَمَ مَا يُخْفِينَ مِن زِينَتِهِنَّ وَتُوبُواْ
إِلَى اللَّهِ جَمِيعاً أَيُّهَ الْمُؤْمِنُونَ لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿31﴾

28. Idan baku sami daya (daga cikin su) ba (dazaiyi muku izini,) to, kadaku ,shige ta saianyi muku izini, inan gaya muku (bayan neman izinin nan) ku koma, to, ku koma, komawar nan Itace tafi Alheri gare, ku (daga zama a kofar gida). Allah masanine da abinda kuke aikatawa (zaiyi muku sakamako a kai).
29. Ba laifi a gareku kushi ga dakuna ba ababan zama ba a cikin ta wacce kuke da amfani a cikin ta, (shine ɓoye jiki da waninsa kamar ɗakunan waƙafi [1] da haimomi abar saki wato rum-funan kasuwa,) Allah yasan abinda kuke bayyanawa da abinda ƙuke ɓoyewa.

(AYAR KULLE)

30. Ka faɗa ga muminai su runtse idandunansu (ga barin abinda duban sa bai halarta su dube shiba,) su kiyaye farjojinsu (ga barin abinda aikatashi bai halatta ba) haƙiƙa ubangiji masanine da abinda suke aikatawa.
31. Ka faɗa ga muminai mataye su runtse idandunansu (ga abinda duban sa bai halatta ba garesu,) su kiyaye farjojinsu (ga barin abinda aikata shi bai halatta ba garesu,) kadasu bayyana adonsu, sai abinda ya bayyana daga gareta, (shine fuska da tafuka guda biyu, ya halatta manisanci yagan shi in ba a tsoron fitina, wurin Imamuna Malik, Allah ya ƙara yarda a gareshi, Imamuna Shafi'i kuwa ya haramta dubansu, Allah ya ƙara yarda a gareshi, saboda gurin zaton fitina ne, wannan ko magana ita aka rinjayar saboda kandagarki,) kuma suyi lullubi da mayafansu, a kan aljihonsu, (wato su suturce kawukansu da ƙirjinsu da mayafai,) kadasu bayyana ɓoyayyen adonsu, (shine abinda ya wanaici fuska da tafuka,) sai ga mazajensu ko iyayensu ko iyayen mazajinsu, ko 'ya'yayensu mazaje, ko 'ya'yayen mazajensu, ko 'yan uwansu ko 'ya'yan 'yan uwansu maza, ko 'ya'yan 'yan uwansu mata ko mata Musulmai 'yan uwansu, ko abinda hannunsu ta mallaka (wato bayinsu, to ya halatta garesu su gan shi, sai abinda yake tsakanin cibiya da gwiwa, to ya haramta ga wanin mazajen aurensu bai halatta su bayyana wa mataye kafirai tsiraicinsu ba wato daga gwiwa zuwa cibiya), ko waɗanda ake cewa dasu (bi nan) wato tsofaffi tukuf, wato waɗanda basa sha'awar mata, ko kuma wawa dulum wato bai rabe tsakanin sama da ƙasa ba, ko mace da namiji, wato, waɗansun ma'abuta bukata daga mazaje wato waɗanda tsiraicinsu baya motsi ko ƙananan yara waƙanda basuyi tsinkaye a kan al'aurar mataye ba, (wato waɗanda basu san meye tarawa da mata ba, to ya halatta su bayyana musu abinda ya wanici cibiya zuwa gwiwa,) kadasuyi bugu da kafafuwansu, don a san abinda suka ɓoye na daga kayan adonsu, (na daga ƙwandage, dasulluwa ko ƙarfen kafa.) Ku tuba izuwa Allah gabaɗayanku yaku waɗannan muminai (daga abinda ya afku gareku na daga duban abinda aka hana ku duban sa da waninsa,) saboda wata kila kwa tsira (daga azabar Allah, wato ya karbi tuban ku).

1).Waƙafi wato sune Mazaunai da aka ginasu saboda ma abota ibada.

وَأَنكِحُواْ الْأَيَٰمَىٰ مِنكُمْ وَالصَّٰلِحِينَ مِنْ عِبَادِكُمْ وَإِمَآئِكُمْ
إِن يَكُونُواْ فُقَرَآءَ يُغْنِهِمُ اللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ وَاللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ﴿32﴾
وَلْيَسْتَعْفِفِ الَّذِينَ لَا يَجِدُونَ نِكَاحًا حَتَّىٰ يُغْنِيَهُمُ اللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ
وَالَّذِينَ يَبْتَغُونَ الْكِتَٰبَ مِمَّا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُكُمْ فَكَاتِبُوهُمْ
إِنْ عَلِمْتُمْ فِيهِمْ خَيْرًا وَءَاتُوهُم مِّن مَّالِ اللَّهِ الَّذِے ءَاتَىٰكُمْ
وَلَا تُكْرِهُواْ فَتَيَٰتِكُمْ عَلَى الْبِغَآءِ إِنْ أَرَدْنَ تَحَصُّنًا لِّتَبْتَغُواْ
عَرَضَ الْحَيَوٰةِ الدُّنْيَا وَمَن يُكْرِههُّنَّ فَإِنَّ اللَّهَ مِنۢ بَعْدِ إِكْرَٰهِهِنَّ
غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿33﴾ وَلَقَدْ أَنزَلْنَا إِلَيْكُمُۥ ءَايَٰتٍ مُّبَيَّنَٰتٍ وَمَثَلًا مِّنَ الَّذِينَ
خَلَوْاْ مِن قَبْلِكُمْ وَمَوْعِظَةً لِّلْمُتَّقِينَ ﴿34﴾ * اللَّهُ نُورُ السَّمَٰوَٰتِ
وَالْأَرْضِ مَثَلُ نُورِهِۦ كَمِشْكَوٰةٍ فِيهَا مِصْبَاحٌ الْمِصْبَاحُ فِے زُجَاجَةٍ الزُّجَاجَةُ
كَأَنَّهَا كَوْكَبٌ دُرِّيٌّ يُوقَدُ مِن شَجَرَةٍ مُّبَٰرَكَةٍ زَيْتُونَةٍ
لَّا شَرْقِيَّةٍ وَلَا غَرْبِيَّةٍ يَكَادُ زَيْتُهَا يُضِيٓءُ وَلَوْ لَمْ تَمْسَسْهُ نَارٌ
نُّورٌ عَلَىٰ نُورٍ يَهْدِے اللَّهُ لِنُورِهِۦ مَن يَشَآءُ وَيَضْرِبُ اللَّهُ الْأَمْثَٰلَ
لِلنَّاسِ وَاللَّهُ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمٌ ﴿35﴾ فِے بُيُوتٍ أَذِنَ اللَّهُ أَن تُرْفَعَ
وَيُذْكَرَ فِيهَا اسْمُهُۥ يُسَبِّحُ لَهُۥ فِيهَا بِالْغُدُوِّ وَالْأٓصَالِ

ربع

(HIKIMAR AURE)

32. Ku aurar da mata marasa mazaje daga cikin ku, (wato 'ya'yaye) da managarta daga bayin kuda kuyangin ku, in su 'ya'yan nan sun kasance fakirai, Allah zai wadata su (albarkacin auren nan) daga falalarsa, Ubangiji mayalwacin baiwa ne (ga halitta) masanine (dasu).

33. Wađanda basu sami abindaza suyi aure dashi ba (na daga sadaki da ciyarwa) su kame kansu (ga barin zina) har Allah ya wadata su daga falalarsa, wađanda suke neman đaura fansa kuwa daga abinda hannun ku ya mallaka (na daga bayi da kuyangi) to, ku đaura musu fansar in kun san alheri a cikinsu, (wato amana da iko a kan kasabi a cikin đaura fansar nan, sigar ta yadda ake yin ta, "Na đaura maka fansa a kan durhami dubu biyu a kan wata biyu, kowane wata dubu daya,, idan ka bani ita to, kai đa ne", yace, "na karɓa", ku basu (ku shiyagabannin nan daga dukiyar Allah wacce ya baku abinda zasu nemi taimakon biyan abinda suka dauka,) kadaku ,tilashi kuyanginku a bisa zina in sun yi nufin katangance kansu don ku nemi đan amfanin rayuwar duniya, (wannan ya afkune cikin Abdullahi dan Ubaiyin da yake tilasa kuyanginsa dasuyi kasabi dazina,) duka wanda ya tilashe su haƙiƙa Ubangiji bayan ya tilashe sun nan mai gafara ne (garesu) mai jinƙai.

34. Haƙiƙa mun saukar mukuda ayoyi mabayyanan ma'anoni da labari mai ban mana ki (shine labarin Nana A'ishatu Allah ya ƙara yarda a gare ta,) daga wađannan da suka wuce gabanku, (kamar labarin Annabi Yusufu da Maryamu) da gargađi ga masu jin tsoron Allah.

(HAƘIƘA TA ANNABI MUHAMMADU TSIRA DA AMINCIN ALLAH YA TABBATA GARESHI)

35. Sarki Allah shine mai haskaka sammai da ƙassai (da hasken rana da watada Annabawa, wađanda suka samu daga hasken manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama,) to, sifar hasken manzon allah (cikin zuciyar mumini) kamar alkuki ne wanda fitila take cikin sa, fitilan nan tana cikin kaskon karau, kaskon karau (alhali hasken yana cikinsa) kai kace tauraro ne mai tsananin haske, da ake hura shi daga itaciya mai albarka, (Itacen zaitun wato bishiyar Atile,) ba bagabashiyaba ba bayamma ba, (wato tana tsakaninsu saboda haka sanyi ko zafi masu cutarwa bazasu dame ta ba,) man ta yana kusa dayayi kyalli, ko da wuta bata shafe shiba, (saboda tsarkinsa,) haske bisa haske, (haskcn wutada hasken Allah, wato shiriyar sa ga mumini haske ne a kan haskcn imani,) Allah yana shiriyar wanda yaga dama izuwa haskensa (wato Dinil-Islam,) Allah yana bayyana misalce-misalce ga mutane (donsuyi izna su bada gaskiya,) Ubangiji masanine da komai.[1]

(TARO SABODA AMBATON UBAN-GUI A MASALLATAI KO WANINTA)

36. Mazaje wađanda saye da sayarwa bata shagalar dasu ga barin ambaton Allah ba (sune masu ambaton Ubangiji a cikin dakuna da Allah yayi izinin a đaukaka su ta wajen gini da wajen ibada, a ambaci sunan sa a cikinta, kuma =

1) Wanda yake so yaga tawilin wannan aya wanda muka rubuta daga farko shine yakomar da lamiri izuwa manzon Allah (S.A.W), to, ya nemi littafin ashafa ta "ALKALA - IYAL" fasalin farko acikin abinda yazo na daga wan-cananka mazaikar yabo da kirari. -Sanajiy -

رِجَالٌ لَّا تُلْهِيهِمْ تِجَارَةٌ وَلَا بَيْعٌ عَن ذِكْرِ اللَّهِ وَإِقَامِ الصَّلَوٰةِ
وَإِيتَآءِ الزَّكَوٰةِ يَخَافُونَ يَوْمًا تَتَقَلَّبُ فِيهِ الْقُلُوبُ وَالْأَبْصَارُ ﴿36﴾
لِيَجْزِيَهُمُ اللَّهُ أَحْسَنَ مَا عَمِلُوا وَيَزِيدَهُم مِّن فَضْلِهِۦ وَاللَّهُ يَرْزُقُ مَن يَشَآءُ
بِغَيْرِ حِسَابٍ ﴿37﴾ وَالَّذِينَ كَفَرُوا أَعْمَالُهُمْ كَسَرَابٍ بِقِيعَةٍ
يَحْسَبُهُ الظَّمْـَٔانُ مَآءً حَتَّىٰ إِذَا جَآءَهُۥ لَمْ يَجِدْهُ شَيْـًٔا وَوَجَدَ اللَّهَ
عِندَهُۥ فَوَفَّىٰهُ حِسَابَهُۥ وَاللَّهُ سَرِيعُ الْحِسَابِ ﴿38﴾ أَوْ كَظُلُمَٰتٍ
فِي بَحْرٍ لُّجِّيٍّ يَغْشَىٰهُ مَوْجٌ مِّن فَوْقِهِۦ مَوْجٌ مِّن فَوْقِهِۦ سَحَابٌ
ظُلُمَٰتٌ بَعْضُهَا فَوْقَ بَعْضٍ إِذَا أَخْرَجَ يَدَهُۥ لَمْ يَكَدْ يَرَىٰهَا وَمَن
لَّمْ يَجْعَلِ اللَّهُ لَهُۥ نُورًا فَمَا لَهُۥ مِن نُّورٍ ﴿39﴾ أَلَمْ تَرَ أَنَّ اللَّهَ يُسَبِّحُ لَهُۥ مَن
فِي السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَالطَّيْرُ صَٰٓفَّٰتٍ كُلٌّ قَدْ عَلِمَ صَلَاتَهُۥ وَتَسْبِيحَهُۥ
وَاللَّهُ عَلِيمٌ بِمَا يَفْعَلُونَ ﴿40﴾ وَلِلَّهِ مُلْكُ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ
ثمن
وَإِلَى اللَّهِ الْمَصِيرُ ﴿41﴾ * أَلَمْ تَرَ أَنَّ اللَّهَ يُزْجِي سَحَابًا ثُمَّ يُؤَلِّفُ بَيْنَهُۥ
ثُمَّ يَجْعَلُهُۥ رُكَامًا فَتَرَى الْوَدْقَ يَخْرُجُ مِنْ خِلَٰلِهِۦ وَيُنَزِّلُ
مِنَ السَّمَآءِ مِن جِبَالٍ فِيهَا مِن بَرَدٍ فَيُصِيبُ بِهِۦ مَن يَشَآءُ وَيَصْرِفُهُۥ
عَن مَّن يَشَآءُ يَكَادُ سَنَا بَرْقِهِۦ يَذْهَبُ بِالْأَبْصَٰرِ

= basa rabkana ga barin tsayar da salla da bada zakka suna jin tsoron rana da zukatada idanduna suke firgita a cikinta, Itace ranar alƙiyama.

37. Don Ubangiji ya saka musu kyakkyawan abinda suka aikata kuma ya kara musu daga falalarsa, Allah yana azurta wanda yaga dama bada lissafi ba. (Waɗanda aka haramta musu hasken Allah, Allah ya kiyashe mu Amin, wato kishiyar waɗanda suke taruwa a kan ambaton Allah).

38. Waɗanda suka kafirta ayyukansu kamar kaluwaiwainiyace a fako da mai jin kishirwa yake zaton ruwa ne har yayin dayazo mata bazai same ta kome ba, zai sami sakamakon Allah nan ga cikinsa, ya cika masa sakamakon (a duniya,) Allah mai gaggawar sakamako ne.

39. Ko (kuma waɗannan da suka kafirta ayyukansu miyagu,) kamar duffai ne a cikin kogi mai zurfi, kumfa yazo masa a birbishin sa kuma akwai wata kumfa, a birbishin kumfar ta biyu akwai girgije, duffai ne sashinta bisa sashi, (duhun kogi da duhun kumfar farko data biyu, da duhun girgije, duhu hudu ke nan). In mai duba yafitar da hannunsa bazai kusa yaganta ba (cikin waɗannan duffai,) wanda Allah bai sa masa haske ba (wato wanda Allah bai shirye shi ba,) to, babu haske a gareshi (wato bazai shiriya ba).

(ABUBUWA DUKKANSU MASU AMBATON UBANGIJI NE DAHARSHEN HALI DANA MAGANA)

40. Shin baka duba cewa lalle Ubangiji duk abinda yake sammai da ƙassai yana ambato gareshi, hakana tsintsaye [1] (tsakanin sama da kasa,) suna masu shinfide fukafukansu, kowane daga cikinsu Allah yasan ganawa tasa da ambatonsa, Allah masanine da abinda suke aikatawa.)

(IKON ALLAH DA JAWUWAR HALITTA GA ALLAH MADAUKAKIN SARKI)

41. Mulkin sammai da ƙassaiya tabbata ga Allah (wato taskokin ruwa da arziki da tsirrai) makomar kowa ta tabbata izuwa ga Allah.

42. Shin baka sani ba cewa Ubangiji shine yake kora girgije a hankali, sannan ya tattara tsakaninsa (wato ya tara sashinsa izuwa sashi, ya mayar dayanke-yankensa wato guntayensa yanki daya,) sannan ua mayer dashi shim, (wato sashinsa bisa sashi,) sai ka ga mana ko yana fitowa daga tsatstsakinsa yana saukar da duwarwatsu na kankara daga sama ya sami wanda yaga damashi, ya juyar dashi ga barin wanda yaga dama, hasken walkiyarsa yana kusata ya tafi da idanduna yana juya dare da rana (wannan ya mayewa wannan,) Lalle a cikin wancananka juyawa akwai izna ga ma'abuta hankula (da zasu gane KuduratulLahi Ta'ala).

1) ya kama jiragen sama saboɗa ba a haɗa faɗin "SAFFATIN" da "WA YAKBIDHNA" ba -Sanajiy

يُقَلِّبُ ٱللَّهُ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَعِبْرَةً لِّأُو۟لِى ٱلْأَبْصَٰرِ ﴿42﴾
وَٱللَّهُ خَلَقَ كُلَّ دَآبَّةٍ مِّن مَّآءٍ فَمِنْهُم مَّن يَمْشِى عَلَىٰ بَطْنِهِۦ
وَمِنْهُم مَّن يَمْشِى عَلَىٰ رِجْلَيْنِ وَمِنْهُم مَّن يَمْشِى عَلَىٰٓ أَرْبَعٍ
يَخْلُقُ ٱللَّهُ مَا يَشَآءُ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿43﴾ لَّقَدْ أَنزَلْنَآ ءَايَٰتٍ
مُّبَيِّنَٰتٍ وَٱللَّهُ يَهْدِى مَن يَشَآءُ إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿44﴾ وَيَقُولُونَ
ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَبِٱلرَّسُولِ وَأَطَعْنَا ثُمَّ يَتَوَلَّىٰ فَرِيقٌ مِّنْهُم مِّنۢ بَعْدِ ذَٰلِكَ
وَمَآ أُو۟لَٰٓئِكَ بِٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿45﴾ وَإِذَا دُعُوٓا۟ إِلَى ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ لِيَحْكُمَ بَيْنَهُمْ
إِذَا فَرِيقٌ مِّنْهُم مُّعْرِضُونَ ﴿46﴾ وَإِن يَكُن لَّهُمُ ٱلْحَقُّ يَأْتُوٓا۟
إِلَيْهِ مُذْعِنِينَ ﴿47﴾ أَفِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ أَمِ ٱرْتَابُوٓا۟ أَمْ يَخَافُونَ
أَن يَحِيفَ ٱللَّهُ عَلَيْهِمْ وَرَسُولُهُۥ بَلْ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿48﴾
إِنَّمَا كَانَ قَوْلَ ٱلْمُؤْمِنِينَ إِذَا دُعُوٓا۟ إِلَى ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ لِيَحْكُمَ
بَيْنَهُمْ أَن يَقُولُوا۟ سَمِعْنَا وَأَطَعْنَا وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ﴿49﴾
وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَيَخْشَ ٱللَّهَ وَيَتَّقْهِ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْفَآئِزُونَ ﴿50﴾
۞ وَأَقْسَمُوا۟ بِٱللَّهِ جَهْدَ أَيْمَٰنِهِمْ لَئِنْ أَمَرْتَهُمْ لَيَخْرُجُنَّ قُل لَّا تُقْسِمُوا۟ ربع
طَاعَةٌ مَّعْرُوفَةٌ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرٌۢ بِمَا تَعْمَلُونَ ﴿51﴾

(ADALCIN UBANGIJI SUBHANAHU WATA'ALA)

43. Ubangiji shine ya halicci dukkan mai rai daga hakika ruwa, (wato hakika r Muhammadu Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama,) akwai daga cikinsu wanda yake tafiya a kan cikinsa (kamar micizai) akwai wanda yake tafiya a kan sawayensa guda biyu (kamar mutum da tsuntsu,) akwai daga garesu wanda yake tafiya a kan sawu hudu (kamar dabbobi, wadansu kuma na tafiya a kan sama da hudu kamar kunami da giza-gizoda shanshani.) Allah yana halittar abında yaga dama (kamar jirgin sama da motada talabijin da kwam fiyutada sauran wa yan daza ayi nan gaba makamancinsu,) hakika Ubangiji mai iko ne bisa komai.)

44. Hakika Mun saukar da ayoyi mabayyana (shine Alkur'ani,) Allah yana shiriyar wanda yaga dama izuwa tafarki madaidaici (wato Dinil-Islam).

45. Munafukai suna cewa mun bada gaskiya da Allah da manzonsa, mun bi (su cikin abinda sukayi hukunci dashi,) sannan sai wadansu mutane daga cikinsu su juya baya bayan wancananka.Wadancananka (masu juya bayan nan) basu kasance muminai ba.

46. Idan an kirawo su izuwa Allah da manzonsa don yayi hukunci tsakaninsu, sai ga wadansu mutane daga cikinsu suna bijirewa (ga barin zuwa gareshi).

47. In ko suna da hakki saisu zo zuwa gareshi suna masu gaggawa.

48. Shin suna da munafunci ne cikin zukatansu ko kuwa suna kokonto ne a cikin annabcinsa, ko suna tsoron Allah da ma'aikinsa suyi zalunci a garesu ne, kai! wadancananka sune hakikanin azzalumai

(FALALAR UBANGIJI SUBHANAHU WATA'ALA)

49. Dahir dai maganar muminai idan an kirawo su izuwa Allah da ma'aikinsa don yayi hukunci tsakaninsu, sukan ce, Munji munbi, wadancananka yayin nan sune hakikanin marabauta.

50. Duk wanda yabi Allah da manzonsa, ya tsoraci Allah ya kiyaye shi, to, hakika wadancananka sune marabauta (da aljanna).

51. Sun rantse da Allah iyakacin rantsuwa Wallahi in ka umarce su (dayaki) lalle zasu fita, cene (dasu) "Ku daina rantsuwa biyayya abar sani (ga manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama Itace tafi daga rantsuwar da bazaku gasgata a kanta ba,) hakika Ubangiji masanine da abinda kuke aikatawa".

قُلْ أَطِيعُوا اللَّهَ وَأَطِيعُوا الرَّسُولَ فَإِن تَوَلَّوْا فَإِنَّمَا عَلَيْهِ
مَا حُمِّلَ وَعَلَيْكُم مَّا حُمِّلْتُمْ وَإِن تُطِيعُوهُ تَهْتَدُوا وَمَا عَلَى
الرَّسُولِ إِلَّا الْبَلَاغُ الْمُبِينُ ﴿52﴾ وَعَدَ اللَّهُ الَّذِينَ ءَامَنُوا مِنكُمْ
وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ لَيَسْتَخْلِفَنَّهُمْ فِي الْأَرْضِ كَمَا اسْتَخْلَفَ الَّذِينَ
مِن قَبْلِهِمْ وَلَيُمَكِّنَنَّ لَهُمْ دِينَهُمُ الَّذِي ارْتَضَىٰ لَهُمْ وَلَيُبَدِّلَنَّهُم
مِّن بَعْدِ خَوْفِهِمْ أَمْنًا يَعْبُدُونَنِي لَا يُشْرِكُونَ بِي شَيْئًا وَمَن
كَفَرَ بَعْدَ ذَٰلِكَ فَأُولَٰئِكَ هُمُ الْفَاسِقُونَ ﴿53﴾ وَأَقِيمُوا الصَّلَوٰةَ
وَءَاتُوا الزَّكَوٰةَ وَأَطِيعُوا الرَّسُولَ لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ ﴿54﴾ لَا تَحْسِبَنَّ
الَّذِينَ كَفَرُوا مُعْجِزِينَ فِي الْأَرْضِ وَمَأْوَاهُمُ النَّارُ وَلَبِئْسَ
الْمَصِيرُ ﴿55﴾ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُوا لِيَسْتَأْذِنكُمُ الَّذِينَ مَلَكَتْ
أَيْمَانُكُمْ وَالَّذِينَ لَمْ يَبْلُغُوا الْحُلُمَ مِنكُمْ ثَلَاثَ مَرَّاتٍ مِّن قَبْلِ
صَلَوٰةِ الْفَجْرِ وَحِينَ تَضَعُونَ ثِيَابَكُم مِّنَ الظَّهِيرَةِ
وَمِن بَعْدِ صَلَوٰةِ الْعِشَاءِ ثَلَاثُ عَوْرَاتٍ لَّكُمْ لَيْسَ عَلَيْكُمْ وَلَا عَلَيْهِمْ
جُنَاحٌ بَعْدَهُنَّ طَوَّافُونَ عَلَيْكُم بَعْضُكُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ
كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ اللَّهُ لَكُمُ الْآيَاتِ وَاللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿56﴾

52. Ccne, "Kubi Allah kubi manzonsa, idan suka bada baya (ga barin da'a,) to haƙiƙa dai abinda yake kansa (na daga iyarwa da aike) shine a kansa, ku kuma abinda aka dora maku (na daga da'a) ne a kanku, in kun bi shi kwa shiriya. Ba kome ga manzo illa ida aike mabayyani".

(DAULAR MUMINAI)

53. Ubangiji ya alƙawarta waɗanda suka bada gaskiya daga cikin ku sukayi aiki nagargaru, lalle zai mayar dasu Khalifofi a cikin ƙasa (maimakon kafirai) tamfar dayasanya waɗanda suke gabansu (na Bani-Isra'ila Khalifofi a maimakon jabberai,) lalle zai tabbatar musu da addininsu, wanda ya yarda dashi garesu (wato addinin Musulunci, shine ya rinjayar dashi a kan dukkan addinai, ya yalwata musu a cikin gamruwa su mallake ta,) lalle zai musanya musu aminci bayan tsoron su (daga kafirai, haƙiƙa Ubangiji ya cika wannan alƙawarin garesu,) da zasu dinga bauta min bazasu shirkanta kome dani ba, to,wanda ya kafirta bayan wancananka (daga gare "u ni'imtawa haƙiƙa wadancananka sune ainihin fasikai, (to farkon wanda ya kafirta dashi wadansu asharārai da suka kashe Sayyadina Usman Allah ya kara yarda a gareshi, dukkan lamari a nan yake, wato kafircewa da ni'imar Allah Itace ta kawo gushewar ta, duk wanda ya gode wa ni'ima ya daure tada dabaibayin ta wanda kuma ya butulce mata yayi kantafi da ita ya nemi gu-shewar ta, kamar yadda Shehu Ibn Ada'illah ya faɗa).

54. Ku tsayar da salla (tareda hakkokin ta ku mika zakka, kubi Allah kubi manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) don ku sami rahamar Allah.

55. Kadaka zaci waɗanda suka butulce wa Allah masu tserewa ne (gare mu) a cikin ƙasa, makomar su (a duniYakunyatada tube mulki, a lahira kuma) wutatirda ita makoma!

(LADUBAN WAƊANDA SUKE ZAUNE A GIDA DAYA)

56. Yaku waɗanda suka bada gaskiya, waɗanda hannun ku ta mallaka (na daga bayi da kuyangi) su nemi izinin kuda waɗanda basu isa balaga badaga cikin ku (na daga 'ya'yaye amma sunsan al'aura da waninta su nemi izinin shigowa gare ku) sau uku, gaban sallar asuba, da lokacin da kuke ajiye tufafin ku daga fatsakin rana (wato lokacin azzahar) da kuma bayan sallar lisha, al'auron uku a gare ku, babu laifi a gareku babu a garesu su yara da magidantan ku (a cikin shiga gareku ba tareda neman izini ba,) bayan waɗannan lokatan guda uku, su masu kewayo ne a kanku (saboda hidima,) ba'alinku mai ke-wayo ne kan ba'ali. kamar yadda aka bayyana muku (abinda aka ambata din nan,) Allah yake muku bayanin ayoyinsa, (ai hukunce-hukuncensa,) Ubangiji masanine (da al'amuran halittarsa) gwanine (cikin abinda ya shirya musu, wannan ayaba shafaffiyaba ce mutane ne dai sukayi sake da ita.)

وَإِذَا بَلَغَ اَ۬لْأَطْفَالُ مِنكُمُ اُ۬لْحُلُمَ فَلْيَسْتَـْٔذِنُواْ كَمَا
اَ۪سْتَـْٔذَنَ اَ۬لَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ اُ۬للَّهُ
لَكُمْ ءَايَٰتِهِۦ وَاللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ (57) * وَالْقَوَٰعِدُ مِنَ اَ۬لنِّسَآءِ
اِ۬لَّٰتِے لَا يَرْجُونَ نِكَاحاً فَلَيْسَ عَلَيْهِنَّ جُنَاحٌ اَن يَّضَعْنَ ثِيَابَهُنَّ
غَيْرَ مُتَبَرِّجَٰتِۭ بِزِينَةٖ وَأَن يَّسْتَعْفِفْنَ خَيْرٞ لَّهُنَّ
وَاللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٞ (58) لَّيْسَ عَلَى اَ۬لْأَعْمَىٰ حَرَجٞ وَلَا عَلَى اَ۬لْأَعْرَجِ
حَرَجٞ وَلَا عَلَى اَ۬لْمَرِيضِ حَرَجٞ وَلَا عَلَىٰٓ أَنفُسِكُمُۥٓ أَن تَأْكُلُواْ
مِنۢ بُيُوتِكُمُۥٓ أَوْ بُيُوتِ ءَابَآئِكُمُۥٓ أَوْ بُيُوتِ اِ۬مَّهَٰتِكُمْ
أَوْ بُيُوتِ إِخْوَٰنِكُمُۥٓ أَوْ بُيُوتِ أَخَوَٰتِكُمُۥٓ أَوْ بُيُوتِ أَعْمَٰمِكُمْ
أَوْ بُيُوتِ عَمَّٰتِكُمُۥٓ أَوْ بُيُوتِ أَخْوَٰلِكُمُۥٓ أَوْ بُيُوتِ خَٰلَٰتِكُمْ
أَوْ مَا مَلَكْتُم مَّفَاتِحَهُۥٓ أَوْ صَدِيقِكُمْ لَيْسَ عَلَيْكُمْ
جُنَاحٌ اَن تَأْكُلُواْ جَمِيعاً اَوَ اَشْتَاتاً فَإِذَا دَخَلْتُم
بُيُوتاً فَسَلِّمُواْ عَلَىٰٓ أَنفُسِكُمْ تَحِيَّةٗ مِّنْ عِندِ اِ۬للَّهِ
مُبَٰرَكَةٗ طَيِّبَةٗ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ اُ۬للَّهُ
لَكُمُ اُ۬لْأٓيَٰتِ لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ (59)

ثمن

57. Idan ƙananan yara daga cikin ku suka isa mafarki (wato balaga,) to, su nemi izni (a cikin dukkan lokatai,) kamar yadda waɗanda suke gaban su (na daga manya-manyan 'ya'yaye) suka nemi izni, (tamfar yadda aka bayyana muku abinda aka ambata) Allah yake bayyana muku ayoyin-sa (wato hukunce-hukuncensa.) Allah masanine (da al'amuran halitta tasa), gwanine (cikin abinda ya shirya musu).

(ALƘUR'ANI YANA KOKAWA DA CI GABA GAMI DA SHA'ANIN MATA)

58. Waɗanda suke zaunannu ga barin haila da haihuwa na daga mataye, waɗanda basa ƙaunar aure (saboda mutuwar sha'awarsu ga barin maza,) to, ba laifi a kansu cewa su yaye tufafinsu, (wato na lullubi,) alhali ba masu bayyanawa da ado ba, (kamar rataye da ƙwandage da ƙarfen ƙafa, waɗanda suke ɓoyayyu,) amma su kame kansu, (wato kadasu yaye lullubin) shine yafi garesu. Allah mai ji ne mai sanine (da abinda yake cikin zukatanku).

(LADABAN MUSULUNCI)

59. Ba laifi a bisa makaho a cikin ciyayya da me gani, ba laifi a bisa gurgu, ba laifi bisa mara lafiya a cikin ciyayya da lafiyayye, ba laifi a kan kawukanku Kuci daga ɗakunanku (wato dakunan 'ya'yanku,) ko daga dakunan iyayenku maza, ko daga dakunan iyayenku mata, ko daga dakunan 'yan uwanku maza, ko daga dakunan 'yan uwanku mata, to daga dakunan baffayinku maza, ko kuwa daga dakunan yagwalgwalolin ku wato nene ko dakunan kawunnan ku, ko dakunan yakunbar ku wato innar ku, ko abinda kuka mallaki mabudansa (wato kuka taskace shi ga waninku,) ko daga dakunan abokan ku (ya halatta Kuci daga dakunan waɗannan da aka ambata ko basa nan in an san bazasu damu ba,) ba laifi gareku Kuci a tattare ko daban daban,(wannan ta sauka ne a cikin wanda ba yason cin abinci shi kadai in bai sami wanda zasu ci tare ba saiyabar cin abincin, wadansu mutane ne da ake ce dasu Banu Laisin, dan Amru daga Bani-Kinanata, dayan su zai zauna bazai ci abinci ba saiya sami bako su ci tare, in bai sami wanda zasu ci tare ba, bazai ci komai ba a rannan) in kun shiga dakunan ku waɗanda ba kowa ciki to kuyi sallama a kan kawukan kukuce Assalamu alaina wa'ala ibadullahis salihina, haƙiƙa Mala'iku sa amsa muku, in akwai kuma mutane kuyi sallama ga mutanen, gaisuwa daga Allah mai albarka mai dadi, daza ayi sakamako a kanta. Irin yadda ya bayyana muku abinda aka ambata din nan hakana Allah yake muku bayanin ayoyinsa don kuyi hankali, ku fahimci wannan.

إِنَّمَا الْمُؤْمِنُونَ الَّذِينَ ءَامَنُوا بِاللَّهِ وَرَسُولِهِ وَإِذَا كَانُوا مَعَهُ عَلَى أَمْرٍ
جَامِعٍ لَّمْ يَذْهَبُوا حَتَّى يَسْتَأْذِنُوهُ إِنَّ الَّذِينَ يَسْتَأْذِنُونَكَ أُولَٰئِكَ
الَّذِينَ يُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ وَرَسُولِهِ فَإِذَا اسْتَأْذَنُوكَ لِبَعْضِ شَأْنِهِمْ
فَأْذَن لِّمَن شِئْتَ مِنْهُمْ وَاسْتَغْفِرْ لَهُمُ اللَّهَ إِنَّ اللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿60﴾
ربع * لَّا تَجْعَلُوا دُعَاءَ الرَّسُولِ بَيْنَكُمْ كَدُعَاءِ بَعْضِكُم بَعْضًا
قَدْ يَعْلَمُ اللَّهُ الَّذِينَ يَتَسَلَّلُونَ مِنكُمْ لِوَاذًا فَلْيَحْذَرِ الَّذِينَ
يُخَالِفُونَ عَنْ أَمْرِهِ أَن تُصِيبَهُمْ فِتْنَةٌ أَوْ يُصِيبَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿61﴾
أَلَا إِنَّ لِلَّهِ مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ قَدْ يَعْلَمُ مَا أَنتُمْ عَلَيْهِ
وَيَوْمَ يُرْجَعُونَ إِلَيْهِ فَيُنَبِّئُهُم بِمَا عَمِلُوا وَاللَّهُ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمٌ ﴿62﴾

25 سُورَةُ الْفُرْقَانِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ سَبْعٌ وَسَبْعُونَ ءَايَةً 77

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

تَبَارَكَ الَّذِي نَزَّلَ الْفُرْقَانَ عَلَىٰ عَبْدِهِ لِيَكُونَ لِلْعَالَمِينَ نَذِيرًا ﴿1﴾
الَّذِي لَهُ مُلْكُ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ وَلَمْ يَتَّخِذْ وَلَدًا وَلَمْ يَكُن
لَّهُ شَرِيكٌ فِي الْمُلْكِ وَخَلَقَ كُلَّ شَيْءٍ فَقَدَّرَهُ تَقْدِيرًا ﴿2﴾

(LADABAN AL'UMMA TAREDA MA'AIKIN ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

60. Haƙiƙa cikakkun muminai kawai sune waɗanda suka bada gaskiya da Allah da manzonsa,idan sun kasance tare dashi a kan wani al'amari mai tarawa kamar hudubar Juma'a bazasu tafi ba saboda wani uzuri dazai bujuro musu sai sun nemi izininsa, wato sukan mike tsaye daura dashi ta indazai ga mutum ya fahimci cewa ya ta shine don neman izini, sai yakan yi wa wanda yaga dama daga cikinsu izini, haƙiƙa waɗanda suke neman izininka sune waɗanda suka bada gaskiya da Allah da mazonsa, in sun nemi izininka saboda ba'alin sha'aninsu, to, yi izini ga wandaka ga dama daga cikinsu.Ka nemi gafarar Allah garesu, haƙiƙa Ubangiji mai gafara ne mai jinkai.

WAJABCIN LADABI AKAN DUKKAN MUSULMI YAYIN KIRAN SUNANSA SALLAL LAHU ALAIHI WASALLAMA WANNAN SHINE BAN GIRMA WANDA ALLAH YACE AYI, BASHIRKA BANE KAMAR YADDA JAHILAN FAHIMTAR ALƘUR'ANI SUKA FADA.

61. Kadaku ,sanya kiran manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama kamar kiran sashin kuda sashi, kadaku ,ce Ya Muhammadu, sai dai ku ce Ya Nabiyyillah, Ya Rasulullah, cikin taushi da twali'u da ƙasƙasta murya. Allah yasan waɗannan dasuke saurarawa daga cikin ku, ai suna fita daga masallaci yayin huduba bada neman izininsa ba a ɓoye, to waɗanda suke saba wa al'amarinsa to suji tsoron cewa masifa zata samesu ko azaba mai radadi a Lahira.

(BARA ZANA DAGA ALLAH IZUWA WAƊANNAN JAHILAN MASU HANA TAWASSULI DA ISTIGASA. WATO:TSANANTUWA DA KAMUN ƘAFA DASHI SALLAL LAHU ALAIHI WASALLAM)

62. Na'am, haƙiƙa abinda yake sammai da ƙassaina Allah ne, haƙiƙa yasan abinda kuke kai na imani da wanin sa, yasan ranar daza a koma daku ,izuwa gareshi, ya labarta musu abinda suka aikata na hairi, ko sharri, Ubangiji masanineshi da komai..

Suratul Furkan

A Makka Aka. Saukar Da Ita Ayoyinta Saba'in Da Bakwai (77)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabaɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

(WANNAN SURATA YI MAGANA KAN TAUHIDI TSANTSA DA ALƘUR'ANI DA ANNABCI DA HALULUWAN ALƘIYAMA, AN CIKA TADA KIRGA SIFOFIN MUMINAI TAMFAR YADDA YA FURTADA TABBATAR DA MAHALICCI GWANI, DA SIFANTASHI DA CIKA. TA YALWATA A CIKIN TAUHIDI TA FIRGITA KAFIRAI, DA AMBATON ƘISSOSHIN AL'UMMA DATA WUCE) "BABU ABIN BAUTAWA DA GASKIYA SAI ALLAH"

1. Sarki daya saukar da Alƙur'ani mai rabewa tsakanin ƙarya da gaskiya, ga bawansa Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi salallama alherinsa ya dadu ya yawaita, domin ya kasance mai gargadi ga talikai, watau mutane da aljannu.
2. Wanda mulkin sammai da ƙassaiya tabbata gareshi, bai riki da ba, bashi da abokin tarayya cikin mulky, ya halicci kowane abu wanda sha"aninsa ne a halicce shi, ya daidaita shi daidaitawa,

وَاتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ ءَالِهَةً لَّا يَخْلُقُونَ شَيْـًٔا وَهُمْ يُخْلَقُونَ
وَلَا يَمْلِكُونَ لِأَنفُسِهِمْ ضَرًّا وَلَا نَفْعًا وَلَا يَمْلِكُونَ
مَوْتًا وَلَا حَيَوٰةً وَلَا نُشُورًا ﴿3﴾ وَقَالَ الَّذِينَ كَفَرُوٓاْ
إِنْ هَٰذَآ إِلَّآ إِفْكٌ افْتَرَىٰهُ وَأَعَانَهُۥ عَلَيْهِ قَوْمٌ ءَاخَرُونَ
فَقَدْ جَآءُو ظُلْمًا وَزُورًا ﴿4﴾ وَقَالُوٓاْ أَسَٰطِيرُ الْأَوَّلِينَ
اكْتَتَبَهَا فَهْيَ تُمْلَىٰ عَلَيْهِ بُكْرَةً وَأَصِيلًا ﴿5﴾ قُلْ أَنزَلَهُ
الَّذِي يَعْلَمُ السِّرَّ فِي السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ إِنَّهُۥ كَانَ غَفُورًا
رَّحِيمًا ﴿6﴾ وَقَالُواْ مَالِ هَٰذَا الرَّسُولِ يَأْكُلُ الطَّعَامَ
وَيَمْشِي فِي الْأَسْوَاقِ لَوْلَآ أُنزِلَ إِلَيْهِ مَلَكٌ فَيَكُونَ مَعَهُۥ
نَذِيرًا ﴿7﴾ أَوْ يُلْقَىٰٓ إِلَيْهِ كَنزٌ أَوْ تَكُونُ لَهُۥ جَنَّةٌ يَأْكُلُ مِنْهَا
وَقَالَ الظَّٰلِمُونَ إِن تَتَّبِعُونَ إِلَّا رَجُلًا مَّسْحُورًا ﴿8﴾
انظُرْ كَيْفَ ضَرَبُواْ لَكَ الْأَمْثَالَ فَضَلُّواْ فَلَا يَسْتَطِيعُونَ سَبِيلًا ﴿9﴾
* تَبَارَكَ الَّذِيٓ إِن شَآءَ جَعَلَ لَكَ خَيْرًا مِّن ذَٰلِكَ جَنَّٰتٍ تَجْرِي
مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَٰرُ وَيَجْعَل لَّكَ قُصُورًا ﴿10﴾ بَلْ كَذَّبُواْ
بِالسَّاعَةِ وَأَعْتَدْنَا لِمَن كَذَّبَ بِالسَّاعَةِ سَعِيرًا ﴿11﴾

ثمن

3. Su kafirai suka riƙi gumaka, ba Allah ba, basu iya halittar komai, sune ma ake halitta, basu mallaki ije cuta ga kansu ba, walajawo amfani, basu mallaki kashe wani ko raya shiba, walaraya matattu.

(RIKICE-RIKICEN KAFIRAI A CIKIN ALƘUR'ANI DA SHA'ANIN ANNABI DA RADDIAKANSU)

4. Waɗanda suka kafirta Sukace, wannan Alƙur'ani bai kasance ba sai ƙarya daya kage ta, wadansu mutane suka taimake shi a kanta wato sune mazowa littafi-Ahlul -Kitabi, haƙiƙa sun aikata kafirci da girbabbiyar ƙarya.
5. Sukace ƙaryace-ƙaryacen mutanen farko ne, yajuye ta daga waɗancananka mutane yajirkita shi, to ita ana karanta masa ita donya haddace ta safiya dayammaci.
6. Ubangiji yayi musu raddi yace, cene, Wanda yasan asirin sammai da ƙassai ne ya saukar dashi, haƙiƙa shiya tabbata mai yawan gafara, mai jinƙai dasu.
7. Sukace Menene ga wannan ma'aiki yake cin abinci, yake tafiya kasuwa, donme ba a saukar da Mala'ika izuwa gareshi baya kasance mai gargadi tare dashi yagasgata shi?

(RIKICE-RIKICENSU DA RADDI A KANSU A CIKIN ALƘUR'ANI DA MA'AIKI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

8. Ko a kawo taska izuwa gareshi daga sama (dazai ciyar dashi, bazai bukata izuwa kasuwa don neman abinci ba,) ko kuwa gona ta kasance gareshi dazai ci daga itaciyar ta (ya wadatar da ita,) Azzalumai (wato kafirai) suka fada (ga muminai) "Ba kwa bi sai mutum abin rinjaye a kan hankalinsa.
9. Duba yaya suka sanya misalce-misalce gareka, (sun kwatanta ka da abin yi wa sihiri kuma da mai buƙata izuwa abindazai ciyar kuma da bukatuwa izuwa Mala'ika dazai tsaya tare dashi a cikin shirya al'amari,) to sai suka bata (ga barin shiriya saboda wancananka)saboda haka bazasu samu damar hanya izuwa shiriya ba.

RADDI KAN KAFIRAI DA BAYANIN HALINSU RANAR ALƘYAMA)

10. Alheri mai yawa ya tabbata ga Allah wanda in yaga dama sai yasanya maka mafi yawa daga wancananka (shine yasanya maka aljannatai) wacce ƙoramu suke kwarara ƙarƙashin ta (a duniya) kuma yasanya maka benaye (bai yi masa haka ba saboda shi yanufi ya bashi waɗannan ƙoramai da benayen a lahira).
11. Sudai bari! Sun ƙaryata da alƙiyama, mun kuma tanaji wuta abar hurawa ga wanda ya ƙaryata ranar alƙiyama

إِذَا رَأَتْهُم مِّن مَّكَانِۢ بَعِيدٖ سَمِعُواْ لَهَا تَغَيُّظاً وَزَفِيراً ﴿12﴾
وَإِذَآ أُلْقُواْ مِنْهَا مَكَاناً ضَيِّقاً مُّقَرَّنِينَ دَعَوْاْ
هُنَالِكَ ثُبُوراً ﴿13﴾ لَّا تَدْعُواْ اُ۬لْيَوْمَ ثُبُوراً وَاحِداً وَادْعُواْ
ثُبُوراً كَثِيراً ﴿14﴾ قُلْ أَذَٰلِكَ خَيْرٌ اَمْ جَنَّةُ اُ۬لْخُلْدِ اِ۬لَّتِے
وُعِدَ اَ۬لْمُتَّقُونَ كَانَتْ لَهُمْ جَزَآءً وَمَصِيراً ﴿15﴾ لَّهُمْ
فِيهَا مَا يَشَآءُونَ خَٰلِدِينَ كَانَ عَلَيٰ رَبِّكَ وَعْداً مَّسْـُٔولاً ﴿16﴾
وَيَوْمَ نَحْشُرُهُمْ وَمَا يَعْبُدُونَ مِن دُونِ اِ۬للَّهِ فَيَقُولُ ءَآنتُمْ
أَضْلَلْتُمْ عِبَادِے هَٰٓؤُلَآءِ أَمْ هُمْ ضَلُّواْ اُ۬لسَّبِيلَ ﴿17﴾ قَالُواْ
سُبْحَٰنَكَ مَا كَانَ يَنۢبَغِے لَنَآ أَن نَّتَّخِذَ مِن دُونِكَ مِنْ أَوْلِيَآءَ
وَلَٰكِن مَّتَّعْتَهُمْ وَءَابَآءَهُمْ حَتَّيٰ نَسُواْ اُ۬لذِّكْرَ وَكَانُواْ
قَوْماً بُوراً ﴿18﴾ فَقَدْ كَذَّبُوكُم بِمَا تَقُولُونَ فَمَا يَسْتَطِيعُونَ
صَرْفاً وَلَا نَصْراً وَمَن يَظْلِم مِّنكُمْ نُذِقْهُ عَذَاباً كَبِيراً ﴿19﴾
وَمَآ أَرْسَلْنَا قَبْلَكَ مِنَ اَ۬لْمُرْسَلِينَ إِلَّآ إِنَّهُمْ لَيَأْكُلُونَ
اَ۬لطَّعَامَ وَيَمْشُونَ فِے اِ۬لْأَسْوَاقِ وَجَعَلْنَا بَعْضَكُمْ
لِبَعْضٖ فِتْنَةً أَتَصْبِرُونَ وَكَانَ رَبُّكَ بَصِيراً ﴿20﴾

12. Idan ta gan su daga guri manisanci sai suji mgugi nata (kamar mai fushi, idan ƙirjinsa ya tafasa daga fushi,) kuma da ƙaraji.
13. Idan aka mguntsuma su a guri mai kunci daga gare ta suna ababan kukumcewa saisu dinga kiran ya halakarsu a cananka (sai a ce dasu);
14. "Kadaku ,kirawo halaka ɗaya, ku kirawo halake-halake masu yawa, (kamar yawan azabar ku").
15. Cene (dasu) "Shin wancananka abin ambato (wato narko da sifar wuta) shine yafi ko aljannar dauwama wacce akayi wa masu tsoron Allah alƙawarinta ta kasance sakamako a garesu (a cikin sanin Allah) da makoma.
16. Abinda suke marmari na garesu a cikin ta suna masu dauwama, wannan alƙawari ya kasance abin roko ga Ubangijinka (ga wanda Allah yayi masa alkawari shine suce Ya UbangijinMukabamu abinda ka alƙawarta mana a bisa harshen manzanninka).

(WANI ABU DAGA SHA'ANUNUWAN RANAR ALƘIYAMA)

17. Ka ambaci ranar da muke tara su da abinda suke bautawa ba Allah ba (na Mala'ikuda Isa da Uzairu) sai Ubangiji ya faɗa (ga ababan bautawar nan don tabbatar da hujja a kan masu bauta). "Shin kune kuka ɓatar da bayina waɗannan (da kuka umarce su da bautar ku,) ko kuwa sune suka bace wa hanyar (gaskiya da kansu?")
18. Sai Sukace, "Tsarki ya tabbatar maka (ga barin abinda bai kamace ka ba,) bai kasance yana kamata garemu mu riƙi waɗansu iyayen giji bakai ba, (yaya zamuyi umarni da a bauta mana,) sai dai kaji dasu dadi ne da iyayensu tun gabansu (da tsawaita ransu dayalwata arziki,) har suka mance gargadi (da bada gaskiya da alƙur'ani) saidai sun kasance mutane halakakku.
19. Haƙiƙa sun karyata ku (wato ababan bautawan nan, sun karyata masu bautan nan, saboda abinda kuke faɗa cewa su iyayen giji ne,) basu ikon juyar da azaba ga barin ku, wala hana muku azabar. Wanda yayi shirka daga cikin ku ma dandana masa azaba mai girma a (lahira).
20. Bamu aiko wani daga manzanni ba gaban ka face su suna cin abinci suna tafiya a cikin kasuwoyi (alhali an gaya musu irin abinda aka fada gareka). Mun sanya ba'alinsu fitina ga ba'ali, (an jarrabi mawadaci da matalauci, mai lafiYakuma da marar lafiya, maɗaukaki da wulaƙantacce, na biyu yana fada a cikin na biyu saboda me bazan zamo kamar na farko ba a cikin komai,) Shin kwa hakura (a kan waɗanda aka jarrabe ku dasu, wato ma'ana ku hakura). Ubangiji kuwa ya tabbata masani (da wandazai daure da wanda zaiyi raki).

(SASHIN WANI ABU DAGA MIYAGUN AYYUKAN KAFIRAI DA AKIBARSA)

حزب

۞ وَقَالَ الَّذِينَ لَا يَرْجُونَ لِقَآءَنَا لَوْلَآ أُنزِلَ عَلَيْنَا الْمَلَٰٓئِكَةُ
أَوْ نَرَىٰ رَبَّنَا لَقَدِ اسْتَكْبَرُوا فِيٓ أَنفُسِهِمْ وَعَتَوْ عُتُوًّا كَبِيرًا ﴿21﴾
يَوْمَ يَرَوْنَ الْمَلَٰٓئِكَةَ لَا بُشْرَىٰ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُجْرِمِينَ وَيَقُولُونَ
حِجْرًا مَّحْجُورًا ﴿22﴾ وَقَدِمْنَآ إِلَىٰ مَا عَمِلُوا مِنْ عَمَلٍ فَجَعَلْنَٰهُ
هَبَآءً مَّنثُورًا ﴿23﴾ أَصْحَٰبُ الْجَنَّةِ يَوْمَئِذٍ خَيْرٌ مُّسْتَقَرًّا وَأَحْسَنُ
مَقِيلًا ﴿24﴾ وَيَوْمَ تَشَقَّقُ السَّمَآءُ بِالْغَمَٰمِ وَنُزِّلَ الْمَلَٰٓئِكَةُ
تَنزِيلًا ﴿25﴾ الْمُلْكُ يَوْمَئِذٍ الْحَقُّ لِلرَّحْمَٰنِ وَكَانَ يَوْمًا عَلَى
الْكَٰفِرِينَ عَسِيرًا ﴿26﴾ وَيَوْمَ يَعَضُّ الظَّالِمُ عَلَىٰ يَدَيْهِ
يَقُولُ يَٰلَيْتَنِي اتَّخَذْتُ مَعَ الرَّسُولِ سَبِيلًا ﴿27﴾ يَٰوَيْلَتَىٰ لَيْتَنِي
لَمْ أَتَّخِذْ فُلَانًا خَلِيلًا ﴿28﴾ لَّقَدْ أَضَلَّنِي عَنِ الذِّكْرِ بَعْدَ
إِذْ جَآءَنِي وَكَانَ الشَّيْطَٰنُ لِلْإِنسَٰنِ خَذُولًا ﴿29﴾ وَقَالَ الرَّسُولُ
يَٰرَبِّ إِنَّ قَوْمِي اتَّخَذُوا هَٰذَا الْقُرْءَانَ مَهْجُورًا ﴿30﴾ وَكَذَٰلِكَ
جَعَلْنَا لِكُلِّ نَبِيٍّ عَدُوًّا مِّنَ الْمُجْرِمِينَ وَكَفَىٰ بِرَبِّكَ هَادِيًا وَنَصِيرًا ﴿31﴾

ثمن

۞ وَقَالَ الَّذِينَ كَفَرُوا لَوْلَا نُزِّلَ عَلَيْهِ الْقُرْءَانُ جُمْلَةً وَٰحِدَةً
كَذَٰلِكَ لِنُثَبِّتَ بِهِۦ فُؤَادَكَ وَرَتَّلْنَٰهُ تَرْتِيلًا ﴿32﴾

21. Wađanda basa kaunar gamuwa da mu (wato basa tsoron tashin alƙiyama) sunce, "Donme ba a saukar da Mala'iku a garemu ba (su kasance jakadu izuwa garemu?) Ko kuwa donme bamu ga Ubangijinmu ba (yabamu labari cewa Annabi Sallallahu alaihi wasallama ma'aikinsa ne?) Haƙiƙa sunyi girman kai a cikin (sha'anin) kawukansu sun tsaga, tsagawa mai girma, (saboda neman su ganin Ubangiji a duniya).

22. Ranar da zasu ga Mala'iku (a cikin jumlar talikai shine ranar Alƙiyama) ba albishir a wannan rana ga kafirai, sabanin mumi-nai, su albishir da aljanna yana garesu,) suna cewa tsari abin tsarewa, (suna neman tsari daga Mala'iku).

23. (Sai Allah mađaukakin Sarki yace,) "Munyi nufi izuwa abinda suka aikata na aikin (alheri, kamar sadaka da sadar da zumuntada agajin firgitacce) kuma muka sanyashi kurar taga abar daidaitawa (a cikin rashin amfani dashi, don ba lada cikin sa, saboda rashin sharadin saza ayi musu sakamako a kansa a duniya).

(WANI ABU DAGA SHA'ANUNUWAN RANAR ALƘIYAMA)

24. "Yan aljanna a wannan rana (ta alƙiyama) sune sukafi kyan. matabbata (daga kafirai a duniya,) sune mafi kyan gurin shakatawa, (wato ƙailula a lokacin da rana ta take. An fahimci ƙarewar hisabi a cikin rabin rana daga wannan kalma kamar yadda yazo a cikin hadisi).

25. Ranar da sama take kyarkecewa tareda (farin) girgije, ana sassaukar da Mala'iku daga sama sassaukarwa (shine Alƙiyama).

26. Mulki a wannan rana ya tabbata ga Arrahamanu, (ba wanda yayi tarayya dashi a cikin sa, a wannan rana) ya kasance. mai tsanani ga kafirai.

27. Kuma ranar da kafiri (wato Ukbatu bn Abi Mu'aiđin yake ciza hannayensa (har ya zuwa murfikansa ko yaushe ya cinye saita fito Yakuma cinyewa, haka za ayi masa) yayi furuci da kalmar shahada sannan ya warware saboda yardar da Ubaiyu dan Khalafu, zai dinga taune wađannan 'yan yatsu zuwa murfukai, don nadama da takaici a ranar alƙiyama,) zai dinga cewa {Dana sani dana riki hanya (ta shiriya) ga manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama)

28. "Ya shiga ukua dana sani da ban riki wan (wato Ubaiyu dan Halafu) badađi ba.

29. " Haƙiƙa ya ɓatar dani ga barin Alƙur'ani, bayan yazo min (shine ya mayar dani ga barin imani dashi".Madaukakin Sarki yace;) "Shaiđan ya kasance mai yawan taɓarwa ga kafiri, (wato ya ɓatar dashi, Yakubuta daga gareshi yayin bala'i).

(ƘAURACE WA ALƘUR'ANI)

30. Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) yace ubangijina ("Haƙiƙa mutanena ƙuraishu) sun riƙi wannan Alƙur'ani abin ƙauracewa, (wannan narko ya shafi dukkan wanda baya ka-rantar Alƙur'ani ba tareda wani dalili ba).

(RARRASHIN MA'AIKI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

31. Kamar yadda Muka sanya magauci gareka na daga mushirikan mutanenka, Muka sanyaga kowane ma'aiki dake gaban ka, (sai ka daure kamar yadda suka daure).Ubangijinka ya isa mai shiryarwa mai taimakon ka (a kan magautan ka).

(HIKIMAR SAUKAR DA ALƘUR'ANI DABAM-DABAN)

32. Wađanda suka kafirta sukace saboda me ba a saukar masa da alƙur'ani gabadayaba (kamar Attaura da Injila da Zabura, Ubangiji yace,) "Mun saukar dashi dabam-daban don mu tabbatar maka da zuciyar ka dashi Muka jera shi jejjerawa (kađankađan don fahintarsa da haddace shiya sauwaka.)

وَلَا يَأْتُونَكَ بِمَثَلٍ إِلَّا جِئْنَاكَ بِالْحَقِّ وَأَحْسَنَ تَفْسِيرًا ﴿33﴾
الَّذِينَ يُحْشَرُونَ عَلَىٰ وُجُوهِهِمْ إِلَىٰ جَهَنَّمَ أُوْلَٰئِكَ شَرٌّ
مَّكَانًا وَأَضَلُّ سَبِيلًا ﴿34﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَى الْكِتَٰبَ
وَجَعَلْنَا مَعَهُ أَخَاهُ هَٰرُونَ وَزِيرًا ﴿35﴾ فَقُلْنَا اذْهَبَا إِلَى
الْقَوْمِ الَّذِينَ كَذَّبُوا بِـَٔايَٰتِنَا فَدَمَّرْنَٰهُمْ تَدْمِيرًا ﴿36﴾ وَقَوْمَ
نُوحٍ لَّمَّا كَذَّبُوا الرُّسُلَ أَغْرَقْنَٰهُمْ وَجَعَلْنَٰهُمْ لِلنَّاسِ ءَايَةً
وَأَعْتَدْنَا لِلظَّٰلِمِينَ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿37﴾ وَعَادًا وَثَمُودَا
وَأَصْحَٰبَ الرَّسِّ وَقُرُونًا بَيْنَ ذَٰلِكَ كَثِيرًا ﴿38﴾ وَكُلًّا
ضَرَبْنَا لَهُ الْأَمْثَالَ وَكُلًّا تَبَّرْنَا تَتْبِيرًا ﴿39﴾ وَلَقَدْ أَتَوْا عَلَى
الْقَرْيَةِ الَّتِي أُمْطِرَتْ مَطَرَ السَّوْءِ أَفَلَمْ يَكُونُوا يَرَوْنَهَا
بَلْ كَانُوا لَا يَرْجُونَ نُشُورًا ﴿40﴾ وَإِذَا رَأَوْكَ إِن يَتَّخِذُونَكَ
إِلَّا هُزُؤًا أَهَٰذَا الَّذِي بَعَثَ اللَّهُ رَسُولًا ﴿41﴾ إِن كَادَ
لَيُضِلُّنَا عَنْ ءَالِهَتِنَا لَوْلَا أَن صَبَرْنَا عَلَيْهَا وَسَوْفَ يَعْلَمُونَ
حِينَ يَرَوْنَ الْعَذَابَ مَنْ أَضَلُّ سَبِيلًا ﴿42﴾ أَرَأَيْتَ مَنِ
اتَّخَذَ إِلَٰهَهُ هَوَاهُ أَفَأَنتَ تَكُونُ عَلَيْهِ وَكِيلًا ﴿43﴾

33. Bazasuzo maka da misali (a cikin ƃata al'amarin ka) ba face Mun zo maka da gaskiya (mai ijewa gareshi) da mafi kyan bayani.

(TAFIYA A KAN FUSKOKI BA A KAN DUGA DUGAI BA)

34. Waɗanda ake kora su a kan fuskokinsu (wato maimakon su tafi a kan sawayensu ana korasu) izuwa jahannama. Waɗancananka sune mafi sharrin mazauni a jahannama mafi bacewar su (ga shiriya, shine kafircinsu da Ubangiji).

(ƘISSOSHIN BA'ALIN AL'UM MA WAƊANDA SUKA ƘARYATA MANZANNI)

35. Haƙiƙa Mun baiwa Annabi Musa Attaura, Mun sanya dan uwansa Harunu waziri a tare dashi (ya taimake shi).

36. Muka ce, "Ku tafi kubiyu izuwa mutane waɗanda suka karyatada ayoyinmu" (wato ƙibɗawa, Fir'auna da mutanensa, suka tafi garesu da aike sai suka karyata su,) sai Muka halakar dasu halakarwa.

37. Ka ambaci mutanen Annabi Nuhu yayir da suka ƙaryata manzanni (wato Annabi Nuhu saboda tsawon zamansa cikin su, kai kace shi manzannine ko saboda cewa karyata shi ƙaryata sauran manzannin ne saboda sunyi tarayya a cikin zuwa da Tauhidi,) yayin da suka ƙaryata manzanni sai Muka nutsar dasu, Muka sanya su izna ga mutane dasuke bayansu, Mun tanaji azaba mai radadi (a lahira) ga kafirai, (banda abinda zai sauka garesu a duniya).

38. Ambaci Adu da Samudu da ma'abota rijiya (mai suna) Rassu (Annabinsu Ance Annabi Shu'aibu ne, Ance hanzatatu ne,suna zaune daura da ita, saita mguza dasu da gidaddajinsu,) da tsareku tsakanin wancananka masu yawa.

39. Kowane daga cikin su mun sanya misali a gareshi (a cikin tsayar da hujja a kansu, bamu haiakar dasu ba sai bayan gargadi). Kowane daya daga garesu Mun halakar dasu halakarwa, (saboda ƙaryatawar su Annabawansu).

40. Haƙiƙa (kafiran Makka) sun wuce bisa alkarya wacce akayi musu mugun ruwa (na duwarwatsu, Itace manya- manyan ga-mruwan mutanen Annabi Luɗu) Shin basu kasance sunaganin ta bane (cikin tafiyar su izuwa Sham, suyi izna?) Bari! Sun kasance basa tsoron Alƙiyama.

(WANI ABU DAGA MIYAGUN AIKACE-AIKACENSU)

41. In sun gan ka basa rikon ka sai abin izgili dashi suna cewa, "Yanzu wannan shine wanda Allah ya aiko manzo?

42. " Haƙiƙa lalle Yakusa ya ƃatar da mu ga barin iyayen -gijinmu ba don mun daure a kanta ba, (Ubangiji yace,) "Da sannu zasu sani zamanin dasuke ganin azaba ƙarara, waye mafi ƃacewa hanya su (ko Muko muminai?")

43. Bani labari wanda ya riƙi son zuciyarsa allansa, shin to kaine zaka kasance wakili a kansa, (da zaka hana shi bin son zuciyarsa? A'a.)



أَمْ تَحْسِبُ أَنَّ أَكْثَرَهُمْ يَسْمَعُونَ أَوْ يَعْقِلُونَ
إِنْ هُمْ إِلَّا كَالْأَنْعَامِ بَلْ هُمْ أَضَلُّ سَبِيلًا ﴿44﴾ * أَلَمْ تَرَ إِلَىٰ
رَبِّكَ كَيْفَ مَدَّ الظِّلَّ وَلَوْ شَاءَ لَجَعَلَهُ سَاكِنًا ثُمَّ جَعَلْنَا
الشَّمْسَ عَلَيْهِ دَلِيلًا ﴿45﴾ ثُمَّ قَبَضْنَاهُ إِلَيْنَا قَبْضًا يَسِيرًا ﴿46﴾
وَهُوَ الَّذِي جَعَلَ لَكُمُ اللَّيْلَ لِبَاسًا وَالنَّوْمَ سُبَاتًا وَجَعَلَ النَّهَارَ
نُشُورًا ﴿47﴾ وَهُوَ الَّذِي أَرْسَلَ الرِّيَاحَ نُشْرًا بَيْنَ يَدَيْ رَحْمَتِهِ
وَأَنزَلْنَا مِنَ السَّمَاءِ مَاءً طَهُورًا ﴿48﴾ لِنُحْيِيَ بِهِ بَلْدَةً مَيْتًا
وَنُسْقِيَهُ مِمَّا خَلَقْنَا أَنْعَامًا وَأَنَاسِيَّ كَثِيرًا ﴿49﴾ وَلَقَدْ صَرَّفْنَاهُ
بَيْنَهُمْ لِيَذَّكَّرُوا فَأَبَىٰ أَكْثَرُ النَّاسِ إِلَّا كُفُورًا ﴿50﴾ وَلَوْ شِئْنَا
لَبَعَثْنَا فِي كُلِّ قَرْيَةٍ نَذِيرًا ﴿51﴾ فَلَا تُطِعِ الْكَافِرِينَ وَجَاهِدْهُم
بِهِ جِهَادًا كَبِيرًا ﴿52﴾ وَهُوَ الَّذِي مَرَجَ الْبَحْرَيْنِ هَٰذَا عَذْبٌ فُرَاتٌ
وَهَٰذَا مِلْحٌ أُجَاجٌ وَجَعَلَ بَيْنَهُمَا بَرْزَخًا وَحِجْرًا مَحْجُورًا ﴿53﴾
وَهُوَ الَّذِي خَلَقَ مِنَ الْمَاءِ بَشَرًا فَجَعَلَهُ نَسَبًا وَصِهْرًا
وَكَانَ رَبُّكَ قَدِيرًا ﴿54﴾ وَيَعْبُدُونَ مِن دُونِ اللَّهِ مَا لَا يَنفَعُهُمْ
وَلَا يَضُرُّهُمْ وَكَانَ الْكَافِرُ عَلَىٰ رَبِّهِ ظَهِيرًا ﴿55﴾

44. Shin ko kana zaton lalle cewa yawancinsu suna ji, (jin fahinta?) ko suna ƙankaltar (abinda kake faɗa?) Su basu kasance ba saitamfar) dabbobi, bari! Su sun fi su bacewar hanya (domin ita tana jawuwa izuwa wanda yake kula da itasu kuwa basa bin Ubangijinsu).

(BA'ALIN ZAHIRORI KASANTATTU)

Ilimin Asdurulab, wato ilimin Agogon rana wanda ake kiran sa a Larabci 'Muzwala' wacce take shiryarwa bisa samuwar Allah da ni'imominsa gare mu.

45. Shin baka duba izuwa aikin Ubangijinka yayaya mika inuwa (wato yayaya shimfiɗa inuwa tun daga lokacin fecewa izuwa hudowar rana) da (Ubangijinka) yaga dama dayasanya matabbaci, (guri ɗaya baza janye saboda hudowar) rana ba, sannan Muka sanya rana dalili a kan wannan inuwa, (badon rana bada baza a san inuwa ba).
46. Sannan Muka tare wannan inuwar shimfiɗaɗɗiya izuwa gare Mu, tarewa kadan (boyayye saɓoda hudowar rana.)
47. Shine wanda ya mayar da dare suttura gareku yasanya bacci hutu gajikkunanku (saboda barin ayyuka) yasanya rana abin ɗaiɗaitawa (a cikin sa wato wuni, saboda neman arziki da waninsa a cikin wunin.)
48. Shine wanda ya sako iskoki ababan ɗaiɗaitawa nan gaba ga rahama ta sa (wato ruwa,) Muka saukar da ruwa mai tsarkakewa daga sama.
49. Don mu rayagari matacce, mu shayar da dabbobi da mutane da yawa (na daga abinda muka halitta da wannan ruwa.)
50. Lalle, Mun rarraba ruwa tsakaninsu domin su wa'azantu, yawaicin mutane sukaki godewa da ni'imar Allah sai kafircewa (da ni'imar dasuke cewa an yi mana ruwa da tauraro kaza).
51. Da Mun ga dama da Mun sanya mai gargaɗi a cikin kowace al'umma (dazai firgita mutanen ta, sai dai mun aiko ka ne izuwa mutanen alƙarya dukkan ta domin ladan ka ya girmama saboda Annabi Sallallahu alaihi wasallama yana da ladan wanda ya bada gaskiya dashi har izuwa ranar alƙiyama).
52. Kadaka daka ta kafirai a cikin son zuciyarsu, ka yake su da Alƙur'ani yaƙi babba.

(WANI ABU DAGA DALILAN TAUHIDI DA KYAKKYAWAR NFIMTAWA DA FUSKANTARWA GA MA'AIKIN ALLAH (SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA) FUSKANTARWA KYAKKYWA)

53. Shine wanda ya saki koguna guda biyu masu makotaka da juna, wannan mai dadi mai zaki, wannan mai zartsi mai kanwa kanwa, yasanya shamaki tsakaninsu ɗayansu (bazai cudanya da daya ba) da tsari abin tsarewa.
54. Shine wanda ya halicci mutum daga maniyyi Ya sanyashi ma'abocin nasaba da surukuta, Ubangijinka ya tabbata mai iko (bisa abinda yaga dama).
55. Kafirai suna bautawa ba Allah ba abinda bazai amfane su ko ya cuce su (da bautarsa ko rashin ta sune gumaka), kafiri ya kasance mai taimakon (shaiɗan) a kan (saɓon) Ubangijinsa.

وَمَا أَرْسَلْنَٰكَ إِلَّا مُبَشِّرًا وَنَذِيرًا ﴿56﴾ قُلْ مَا أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ
مِنْ أَجْرٍ إِلَّا مَن شَآءَ أَن يَتَّخِذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ سَبِيلًا ﴿57﴾ وَتَوَكَّلْ
عَلَى ٱلْحَيِّ ٱلَّذِي لَا يَمُوتُ وَسَبِّحْ بِحَمْدِهِۦ وَكَفَىٰ بِهِۦ بِذُنُوبِ
عِبَادِهِۦ خَبِيرًا ﴿58﴾ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ
وَمَا بَيْنَهُمَا فِي سِتَّةِ أَيَّامٍ ثُمَّ ٱسْتَوَىٰ عَلَى ٱلْعَرْشِ
ٱلرَّحْمَٰنُ فَسْـَٔلْ بِهِۦ خَبِيرًا ﴿59﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ ٱسْجُدُوا۟
لِلرَّحْمَٰنِ قَالُوا۟ وَمَا ٱلرَّحْمَٰنُ أَنَسْجُدُ لِمَا تَأْمُرُنَا وَزَادَهُمْ
نُفُورًا * ﴿60﴾ * تَبَارَكَ ٱلَّذِي جَعَلَ فِي ٱلسَّمَآءِ بُرُوجًا وَجَعَلَ سجدة ثمن
فِيهَا سِرَٰجًا وَقَمَرًا مُّنِيرًا ﴿61﴾ وَهُوَ ٱلَّذِي جَعَلَ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ
خِلْفَةً لِّمَنْ أَرَادَ أَن يَذَّكَّرَ أَوْ أَرَادَ شُكُورًا ﴿62﴾ وَعِبَادُ
ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلَّذِينَ يَمْشُونَ عَلَى ٱلْأَرْضِ هَوْنًا وَإِذَا خَاطَبَهُمُ ٱلْجَٰهِلُونَ
قَالُوا۟ سَلَٰمًا ﴿63﴾ وَٱلَّذِينَ يَبِيتُونَ لِرَبِّهِمْ سُجَّدًا وَقِيَٰمًا ﴿64﴾
وَٱلَّذِينَ يَقُولُونَ رَبَّنَا ٱصْرِفْ عَنَّا عَذَابَ جَهَنَّمَ إِنَّ عَذَابَهَا
كَانَ غَرَامًا ﴿65﴾ إِنَّهَا سَآءَتْ مُسْتَقَرًّا وَمُقَامًا ﴿66﴾ وَٱلَّذِينَ إِذَآ
أَنفَقُوا۟ لَمْ يُسْرِفُوا۟ وَلَمْ يَقْتُرُوا۟ وَكَانَ بَيْنَ ذَٰلِكَ قَوَامًا ﴿67﴾

56. Bamu aiko ka ba face mai albishir da (gidan aljanna,) mai gargaɗi da (wuta).

57. Cene (dasu) "Ban tambaye ku lada bisa ida aikena ba, kai dai wanda yaga dama zai riki hanya ta tsira izuwa Ubangijinsa (da ciyar da dukiyarsa a cikin neman yardar Allah, to bazan hana shi wannan ba).

58. Kai dai yi dogaro a kan rayayyc wanda bazai mutu ba, ka ce, "SUBHANALLAHI WAL HAMDU LILLAHI" ya isa mai cikakken sani da zunuban bayinsa.

(HIKIMAR YIN SANNU-SANNU A CIKIN AL'AMURA)

59. Shine wanda ya halicci sammai da ƙassaida abinda yake tsakaninsu a cikin miƙdarin kwana shida (Ance miƙdari saboda a lokacin ba rana ba wata. D? yaga dama da saiya halicce su a cikin ƙiftawar ido, yayi haka ne saboda yasanar da halittayi a sannu a sannu), sannan yayi daidaito a kan Al'arshi shine ARRAHAMANU Sarki mai yawan jinƙai (daidaito wanda ya kamace shi). To ka tambayi masani dashi (ARRAHAMANU ya baka labari da sifofinsa.)

(WAJABCIN SANIN TAUHIDI)

60. In akace dasu "Kuyi sujada ga Ubangiji Arrahamanu", saisu ce, "Me ye ARRAHAMANU" (suna zaton Musailamatul ƙazzabu), yaya zamuyi sujada ga abinda kake umarninmu (wato suna nufin Annabi Sallallahu alaihi wasallama, bamu sanshi ba, bazamuyi sujada gareshi ba,) wannan magana saita ƙara musu nisa (ga barin imani).

61. Ubangiji, Sarkin nan dayasanya burujai goma sha biyu a cikin sama alherinsa ya dadu ya yawaita (Hamalu, Saum, Jauza'u, Saraɗanu, Asadu, sunbala Mizanu, Aƙrabu, ƙausu, Jadyu, Dalwu, Hutu Itacc manzilolin taurari bakwai matafiya. Murrikha yana da Hamalu da Aƙrabu, Zuhara tana da Sauru da Mizanu, Uɗaridu yana da Jauza'u dasumbula, ƙamaru yana da Saraɗanu, Shamsu tana da Asadu, Mushtari yana da ƙausu da Hutu, Zuhal yana da Jadyu da Dalwu). Yasanyafitila mai haske a cikin ta (wato rana da wata mai haske.

62. Shine wanda yasanya dare da rana mayau ga wanda yakc nufin ya wa'azantu ko yake nufin godiyar ni'imar Ubangiji.

(SHARUDDAN DARIKOKIN SUFAYE GABADAYA)

63. Bayin Ubangiji Arrahamnu (mubtada ne, labarinsa aya ta saba'in da biyar (75) abinda ke tsakaninsu kuma sifofin mubtada ne) waɗanda suke tafiya a nutse a ƙasƙasce (bada takabbura ba) idan jahilai sun yi zancc dasu, sai sukan faɗa musu magana ta lumana bada tashin hankali ba[1]

64. Waɗanda suke kwana suna sujada ga Ubangijinsu suna masu ƙiyamul -laili (sallar tsakar dare),

65. Da waɗanda suke cewa "Ya Ubangijinmu juyar da azabar jahannama ga barin mu, haƙiƙa azabata ta kasance dolc.

66. " Haƙiƙa ita ta mugusta matabbaci da mazauni".

67. Da waɗanda idan suka ciyar (ga iyalinsu) baza suyi barna ba baza suyi kwauro ba, ciyarwar tasu zata kasance tsakanin wancananka barna da kwauro.

1) wato basa saka sayyi'a da sayyi'a, wannan ta'ada tana daga mafi girman tadoli saboda abinda yakc cikin hadisi" Mai hakuri Yakusa ya zama Annabi - Sanajiy -

وَالَّذِينَ لَا يَدْعُونَ مَعَ اللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ وَلَا يَقْتُلُونَ
النَّفْسَ الَّتِي حَرَّمَ اللَّهُ إِلَّا بِالْحَقِّ وَلَا يَزْنُونَ
وَمَن يَفْعَلْ ذَٰلِكَ يَلْقَ أَثَامًا ﴿68﴾ يُضَٰعَفْ لَهُ الْعَذَابُ
يَوْمَ الْقِيَٰمَةِ وَيَخْلُدْ فِيهِ مُهَانًا ﴿69﴾ إِلَّا مَن تَابَ
وَءَامَنَ وَعَمِلَ عَمَلًا صَٰلِحًا فَأُوْلَٰٓئِكَ يُبَدِّلُ اللَّهُ سَيِّـَٔاتِهِمْ
حَسَنَٰتٍ وَكَانَ اللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿70﴾ وَمَن تَابَ وَعَمِلَ
صَٰلِحًا فَإِنَّهُ يَتُوبُ إِلَى اللَّهِ مَتَابًا ﴿71﴾ وَالَّذِينَ
لَا يَشْهَدُونَ الزُّورَ وَإِذَا مَرُّوا بِاللَّغْوِ مَرُّوا كِرَامًا ﴿72﴾
وَالَّذِينَ إِذَا ذُكِّرُوا بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمْ لَمْ يَخِرُّوا عَلَيْهَا
صُمًّا وَعُمْيَانًا ﴿73﴾ وَالَّذِينَ يَقُولُونَ رَبَّنَا هَبْ لَنَا
مِنْ أَزْوَٰجِنَا وَذُرِّيَّٰتِنَا قُرَّةَ أَعْيُنٍ وَاجْعَلْنَا
لِلْمُتَّقِينَ إِمَامًا ﴿74﴾ أُوْلَٰٓئِكَ يُجْزَوْنَ الْغُرْفَةَ بِمَا صَبَرُوا
وَيُلَقَّوْنَ فِيهَا تَحِيَّةً وَسَلَٰمًا ﴿75﴾ خَٰلِدِينَ فِيهَا
حَسُنَتْ مُسْتَقَرًّا وَمُقَامًا ﴿76﴾ قُلْ مَا يَعْبَؤُا بِكُمْ رَبِّي
لَوْلَا دُعَآؤُكُمْ فَقَدْ كَذَّبْتُمْ فَسَوْفَ يَكُونُ لِزَامًا ﴿77﴾

68. Da waɗanda basa bautawa wani tareda Allah basa kisan kai wacce Allah ya haramta ga kashe ta saida gaskiya, basa zina. Wanda ya aikata wanca-nanka (daya daga waɗannan ukun) zai gamu da uƙuba.

69. Za a ninka masa azaba ranar Alƙiyama, zai dauwama a cikin ta abin wulaƙantawa.

70. Sai wanda ya tuba ya bada gaskiya ya aikata aiki na gari daga cikin su, waɗancananka Allah musanya miyagun ayyukansu kyawawa (a Lahira,) Ubangiji ya tabbata mai gafara mai yawan jinƙai.

71 Wanda ya tuba daga zunubai, (ban da waɗanda aka ambata,) yayi aiki na gari, haƙiƙa zai koma ga Allah komawa kyakkyawa, (Ubangiji zaiyi masa kyakkyawan sakamako).

(HARSASHIN DARIKAR ƘADIRIYA)

72. Da waɗanda basa shaidar zir, idan sun wuce ga zancen banza, sukan wuce suna masu girma, (wato sukan bijire ga barin sa).

73. Da waɗanda in an gargaɗe su da ayoyin Ubangijinsu (Alƙur'ani) bazasu faɗo a kansa suna kurama ba, makafi (bari zasu faɗo masuji masu amfani).

74. Da waɗanda suke cewa, "Ya Ubangijinmu bamu sanyin idaniya daga matayenmu da zurriyarmu, (sune mu gan su suna masu biyayya a gareka,) ka sanya mu limana i ga masu tsoron Allah (a cikin- alheri)"

75. Waɗancananka ana saka musu benaye (a cikin aljanna) saboda dauriyarsu (bisa ɗa'ar Allah,) ana gama su da gaisuwa da jinjina daga Mala'iku a cikin (ita benayen).

76. Halin kasancewar su masu dauwama a cikin ta, ta kyautata matabbaci da madawwami.

(FALALAR ADDITA)

77. Ka faɗa (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama ga mutanen Makka,) Ubangijina bazai kula daku ,ba. Ba don rokon Sa da kuke (cikin tsanance-tsanance, ya yaye muku ita) ba yaya zai kula daku alhali kuna ƙaryatawa (da manzo da Alƙur'ani!) Da sannu (azaba) zata kasance (gareku) dole (a Lahira, bayan abinda zaisame ku a duniya na daga masifofi, aka kashe saba'in daga garesu a ranar Badar).

26 سُورَةُ الشُّعَرَاءِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ مِائَتَانِ وَسَبْعٌ وَعِشْرُونَ ءَايَةً 227

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

رُبع

* طسٓمٓ ﴿١﴾ تِلْكَ ءَايَٰتُ الْكِتَٰبِ الْمُبِينِ ﴿٢﴾ لَعَلَّكَ بَٰخِعٌ نَّفْسَكَ
أَلَّا يَكُونُواْ مُؤْمِنِينَ ﴿٣﴾ إِن نَّشَأْ نُنَزِّلْ عَلَيْهِم مِّنَ السَّمَآءِ ءَايَةً فَظَلَّتْ
أَعْنَٰقُهُمْ لَهَا خَٰضِعِينَ ﴿٤﴾ وَمَا يَأْتِيهِم مِّن ذِكْرٍ مِّنَ الرَّحْمَٰنِ مُحْدَثٍ
إِلَّا كَانُواْ عَنْهُ مُعْرِضِينَ ﴿٥﴾ فَقَدْ كَذَّبُواْ فَسَيَأْتِيهِمْ أَنۢبَٰٓؤُاْ مَا كَانُواْ بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿٦﴾
أَوَلَمْ يَرَوْاْ إِلَى الْأَرْضِ كَمْ أَنۢبَتْنَا فِيهَا مِن كُلِّ زَوْجٍ كَرِيمٍ ﴿٧﴾
إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَءَايَةً وَمَا كَانَ أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿٨﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ الْعَزِيزُ الرَّحِيمُ ﴿٩﴾
وَإِذْ نَادَىٰ رَبُّكَ مُوسَىٰٓ أَنِ ائْتِ الْقَوْمَ الظَّٰلِمِينَ ﴿١٠﴾ قَوْمَ فِرْعَوْنَ أَلَا يَتَّقُونَ ﴿١١﴾
قَالَ رَبِّ إِنِّيٓ أَخَافُ أَن يُكَذِّبُونِ ﴿١٢﴾ وَيَضِيقُ صَدْرِي وَلَا يَنطَلِقُ لِسَانِي
فَأَرْسِلْ إِلَىٰ هَٰرُونَ ﴿١٣﴾ وَلَهُمْ عَلَيَّ ذَنۢبٌ فَأَخَافُ أَن يَقْتُلُونِ ﴿١٤﴾ قَالَ كَلَّا
فَاذْهَبَا بِـَٔايَٰتِنَآ إِنَّا مَعَكُم مُّسْتَمِعُونَ ﴿١٥﴾ فَأْتِيَا فِرْعَوْنَ فَقُولَآ إِنَّا رَسُولُ رَبِّ
الْعَٰلَمِينَ ﴿١٦﴾ أَنْ أَرْسِلْ مَعَنَا بَنِيٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ﴿١٧﴾ قَالَ أَلَمْ نُرَبِّكَ فِينَا وَلِيدًا وَلَبِثْتَ
فِينَا مِنْ عُمُرِكَ سِنِينَ ﴿١٨﴾ وَفَعَلْتَ فَعْلَتَكَ الَّتِي فَعَلْتَ وَأَنتَ مِنَ الْكَٰفِرِينَ ﴿١٩﴾

Suratu-s Shu'ara'i

A Makka Aka. Saukar Da Ita Ayoyinta Dari Biyu. Da Ishirin Da Bakwai (227)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabaɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

Wannan sura ta tattarar bisa rarrashin Ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wasallama da ƙissoshin Annabawa da kirari da Alƙur'ani dayadda yake a gurin mushurikai da nasihohi da aka fuskantar dasu izuwa ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wasallama, don jama'a tasa dayadda ake Huluri a cikin sallah da wanin tada raddi a kan mai sifanta Annabi da bokanci ko waka da kirari ga mawaka na Ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wasallama, kamar Hassanu da Alfazazi da Bura'i da Nabahani da sauransu Allah ya yarda a garesu'.

(RARRASHIN ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

1. D.H.S.M. (Allahu a'alamu bi-mu-radihi-bi-zalika.) Waɗannan ayoyi ayoyin Alƙur'ani ne mai bayyana ƙarya da gaskiya.
2. Wata kila kai (Ya Muhammadu Sallallahu alaika wasallama) mai halakar da kanka ne don bakin ciki saboda mutanen Makka basu bada gaskiya ba!
3. In mun ga dama zamu saukar da azaba a kansu daga sama, wuyayunsu su zamo maƙasƙanta don ta, (wato idonsu ya raina fata).
4. Babu wani abu dazaizo musu na daga ƙur'ani saboda daga Sarki Arrahamanu, face sai sun kasance masu bijirewa gareshi.
5. To, haƙiƙa sun ƙaryata dashi, to da sannu aƙibar abinda suke izgili dashi zai sauka garesu.
6. Shin basu duba izuwa ƙasa ba nawa ne muka saukar da dukkan nau'i kyakkyawa?
7. Haƙiƙa lalle akwai aya cikin wan-cananka mai shiryarwa a bisa cikakken ikon Ubangiji, yawancinsu basu kasance masu bada gaskiya ba a cikin sanin Allah.
8. Haƙiƙa Ubangijinka lalle shine mabuwayi (ga kafirai) mai jinƙai (ga muminai, zaiyi wa kafirai azaba yayi wa muminai jinƙai).

(ƘISSAR ANNABI MUSA ALAIHISSALAM) DA ABINDA TA KUNSA NA DAGA MUHAWARORI DA KURKU KUNFIR'AUNA. (WATO ƘAREKU - KANKA)

9. Ka ambata (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama ga mutanenka) zamanin da Ubangijinka ya kira Annabi Musa dayaga (wuta ga itaciya) cewa ka je wa mutane azzalumai kana manzo izuwa garesu.
10. Mutanen Fir'auna (tareda Fir'auna din) sun zalinci kansu tareda Allah, sun zalinci Bani-Isra'ila da bautar dasu,) Shin basa jin tsoron Allah (da da'a tasa su kaɗai ta Shi?)
11. Annabi Musa (Alaihissalamu) yace, "Ubangijina ina tsoron su karyatani!
12. Kirjina Yakuntata daga ƙaryatawar su gare ni kuma harshena yaki sakuwa da isar da aike (saboda guragurar da take cikinsa), kayi aike izuwa dan uwana Haruna tareda ni!
13. Suna da laifi a kaina (na kashe Baƙibɗe na wajen su,) ina jin tsoron su kashe ni (saboda shi).
14. Ubangiji ta'ala yace, "Bazasu kashe ka ba sai ka tafi kai da dan uwanka da ayoyinmu, haƙiƙa Mu Muna taredaku ,munajin (abinda kuke faɗa da abinda ake faɗa muku.)
15. Ku je wa Fir'auna ku ce masa, " Haƙiƙa Mu jakadun Ubangijin talikaine (izuwa gareka).
16. Cewa bamu Bani-Isra'ila mu tafi dasu Sham.
17. Sai Fir'auna yace (da Annabi Musa alaihissalam) "Shin bamu raine ka bane a cikin gidadda-jinmu kana dan kankanin yaro kusa da haihuwa bayan yaye, ka zauna cikinmu (shekaru talatin (30) kana daura tufar Fir'auna kana hawa dawakansa ana kuma ambaton ka dansa?)
18. "Ka aikata aika-aikarka wacce ka aikata (shine kisan Bakibde,) alhali kana daga cikin masu butulcewa (ni'imata a kanka, da raino, da rashin bautarwa).

قَالَ فَعَلْتُهَا إِذاً وَأَنَا مِنَ الضَّالِّينَ ﴿19﴾ فَفَرَرْتُ مِنكُمْ لَمَّا
خِفْتُكُمْ فَوَهَبَ لِي رَبِّي حُكْماً وَجَعَلَنِي مِنَ الْمُرْسَلِينَ ﴿20﴾ وَتِلْكَ
نِعْمَةٌ تَمُنُّهَا عَلَيَّ أَنْ عَبَّدتَّ بَنِي إِسْرَآءِيلَ ﴿21﴾ * قَالَ فِرْعَوْنُ
وَمَا رَبُّ الْعَالَمِينَ ﴿22﴾ قَالَ رَبُّ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا إِن كُنتُم
مُّوقِنِينَ ﴿23﴾ قَالَ لِمَنْ حَوْلَهُ أَلَا تَسْتَمِعُونَ ﴿24﴾ قَالَ رَبُّكُمْ وَرَبُّ
ءَابَآئِكُمُ الْأَوَّلِينَ ﴿25﴾ قَالَ إِنَّ رَسُولَكُمُ الَّذِي أُرْسِلَ إِلَيْكُمْ
لَمَجْنُونٌ ﴿26﴾ قَالَ رَبُّ الْمَشْرِقِ وَالْمَغْرِبِ وَمَا بَيْنَهُمَا إِن كُنتُمْ
تَعْقِلُونَ ﴿27﴾ قَالَ لَئِنِ اتَّخَذْتَ إِلَٰهاً غَيْرِي لَأَجْعَلَنَّكَ مِنَ
الْمَسْجُونِينَ ﴿28﴾ قَالَ أَوَلَوْ جِئْتُكَ بِشَيْءٍ مُّبِينٍ ﴿29﴾ قَالَ فَأْتِ بِهِ
إِن كُنتَ مِنَ الصَّادِقِينَ ﴿30﴾ فَأَلْقَىٰ عَصَاهُ فَإِذَا هِيَ ثُعْبَانٌ
مُّبِينٌ ﴿31﴾ وَنَزَعَ يَدَهُ فَإِذَا هِيَ بَيْضَآءُ لِلنَّاظِرِينَ ﴿32﴾ قَالَ لِلْمَلَإِ
حَوْلَهُ إِنَّ هَٰذَا لَسَاحِرٌ عَلِيمٌ ﴿33﴾ يُرِيدُ أَن يُخْرِجَكُم مِّنْ أَرْضِكُم
بِسِحْرِهِ فَمَاذَا تَأْمُرُونَ ﴿34﴾ قَالُوا أَرْجِهِ وَأَخَاهُ وَابْعَثْ
فِي الْمَدَآئِنِ حَاشِرِينَ ﴿35﴾ يَأْتُوكَ بِكُلِّ سَحَّارٍ عَلِيمٍ ﴿36﴾ فَجُمِعَ السَّحَرَةُ
لِمِيقَاتِ يَوْمٍ مَّعْلُومٍ ﴿37﴾ وَقِيلَ لِلنَّاسِ هَلْ أَنتُم مُّجْتَمِعُونَ ﴿38﴾

ثمن

19. Annabi Musa yace, Na aikata yayin nan alhali ina cikin masu kuskure ba masu ganganciba (ga barin abinda Allah ya bani bayan ta na daga ilimi da aike).
20. "Saina gudu daga gareku yayin da naji tsoron ku, sai Ubangijina ya bani ilimi yasanya ni cikin mursalansa.
21. "Wancananka ni'ima ce da kake goranta min ita, ka bautar da Bani-Isra'ila, (baka bautar dani ba, ba gori a gare ni saboda wannan, saboda ka zalunce sune daka bautar dasu").
22. Sai Fir'auna yace (da Annabi Musa Alaihissalamu,) "Me ye Ubangijin talikai "wanda kace kai ma'aikinsa ne, ai wane abu ne shi? (ayayin dayazama babu wata hanyaga halitta Alaihissalatu wassalamu wani hanyaga taliki izuwa sanin haƙiƙar Ubangiji sai dai a sanshi da sifofinsa, sai Annabi Musa ya amsa ba'alin sifofinsa).

(SANIN ALLAH TA KAN SIFOFINSA)

23. Yace, "Ubangijin sammai da kassaida abinda yake tsakanin su (shine mahaliccin su,) in kun kasance masu amincewa,(da cewa shine mahaliccin su to ku bada gaskiya dashi ku kadaita shi).
24. Fir'auna yace da waɗanda suke daura dashi (manyan mutanensa,) "Shin ba kwa jin (jawabinsa wanda bai dace da tambaya ba?)
25. Sai (Annabi Musa Alaihissalamu) yace, "Ubangijinku, ubangijin iyayen ku na farko (ko ya yake ya shiga cikin abinda yake gaban sa wannan, sab zai bakanta wa Fir'auna saboda haka.)
26. (Sai Fir'auna) yace, " Haƙiƙa manzon nan nakuda aka aiko muku zuwa gareku lalle mahaukaci ne.
27. (Sai Musa) yace, "Ubangijin mahudar rana da mafadar tada abinda yake tsakanin su in kun kasance kuna hankaltacewa shi mahaliccinsune shi, to ku bada gaskiya dashi ku kaɗaita shi.

(KURKUKUN FIR'AUNA)

28. Sai Fir'auna yace da Annabi Musa Alaihissalamu, Wallahi in ka riƙi ubangiji bani ba tabbas ne zan sanya ka cikin ababan ɗaurewa, kurkukunsa mai tsanani ne, yana ɗaure mutum a ƙarƙashin ƙasa bazai ga kowa ba, bazaiji kowa ba.
29. Sai Annabi Musa alaihissalamu yace, Shin kayi haka koda nazo maka da wani abu mabayyani wato dalili a kan jakadancina?
30. Fir'auna yace dashi zo dashi in ka kasance magasgaci cikinta.
31. Sai Annabi Musa (Alaihissalamu) ya yada sandarsa saita zama micijiya babba.
32. Yafitar da hannunsa (daga alji-hunsa) sai ga ta fara mai kyalkyali ga masu duba, (sabanin abinda take kai naja).
33. Sai Fir'auna ya faɗa ga manyan mutanensa dake daura dashi, " Haƙiƙa wannan lalle matsafi ne wanda ba irin sa a sanin tsafi.
34. "Yana nufin yafitar daku ,daga kasarkuda sanin tsafin, to wane abu kukc shawara?"
35. Sukace, "Jinkirta" (shi da dan uwansa) ka tura masu tattaro matsafa a garuruwa,
36. Su zo maka da dukkan tsafau wanda yafi kowa a cikin sanin tsafi".
37. Aka tara matsafa ga mikatin rana abin sani (shine lokacin walaha na ranar ado.)
38. Akace da mutane, Ba kwa tattaraba,

لَعَلَّنَا نَتَّبِعُ اُ۬لسَّحَرَةَ إِن كَانُواْ هُمُ اُ۬لْغَٰلِبِينَ ﴿39﴾ فَلَمَّا جَآءَ اَ۬لسَّحَرَةُ
قَالُواْ لِفِرْعَوْنَ أَٰيِنَّ لَنَا لَأَجْراً اِن كُنَّا نَحْنُ اُ۬لْغَٰلِبِينَ ﴿40﴾ قَالَ نَعَمْ
وَإِنَّكُمْ إِذاً لَّمِنَ اَ۬لْمُقَرَّبِينَ ﴿41﴾ قَالَ لَهُم مُّوسَىٰ أَلْقُواْ مَا أَنتُم مُّلْقُونَ ﴿42﴾
فَأَلْقَوْاْ حِبَالَهُمْ وَعِصِيَّهُمْ وَقَالُواْ بِعِزَّةِ فِرْعَوْنَ إِنَّا لَنَحْنُ
اُ۬لْغَٰلِبُونَ ﴿43﴾ فَأَلْقَىٰ مُوسَىٰ عَصَاهُ فَإِذَا هِيَ تَلْقَفُ مَا يَأْفِكُونَ ﴿44﴾
فَأُلْقِيَ اَ۬لسَّحَرَةُ سَٰجِدِينَ ﴿45﴾ قَالُواْ ءَامَنَّا بِرَبِّ اِ۬لْعَٰلَمِينَ ﴿46﴾
رَبِّ مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ ﴿47﴾ قَالَ ءَآمَنتُمْ لَهُۥ قَبْلَ أَنْ ءَاذَنَ لَكُمُۥٓ
إِنَّهُۥ لَكَبِيرُكُمُ اُ۬لذِے عَلَّمَكُمُ اُ۬لسِّحْرَ فَلَسَوْفَ تَعْلَمُونَ ﴿48﴾ لَأُقَطِّعَنَّ
أَيْدِيَكُمْ وَأَرْجُلَكُم مِّنْ خِلَٰفٖ وَلَأُوصَلِّبَنَّكُمُۥٓ أَجْمَعِينَ ﴿49﴾ * قَالُواْ لَا ضَيْرَ
إِنَّا إِلَيٰ رَبِّنَا مُنقَلِبُونَ ﴿50﴾ إِنَّا نَطْمَعُ أَنْ يَّغْفِرَ لَنَا رَبُّنَا خَطَٰيَٰنَا أَن
كُنَّا أَوَّلَ اَ۬لْمُؤْمِنِينَ ﴿51﴾ وَأَوْحَيْنَا إِلَيٰ مُوسَىٰ أَنِ اِسْرِ بِعِبَادِے
إِنَّكُم مُّتَّبَعُونَ ﴿52﴾ فَأَرْسَلَ فِرْعَوْنُ فِے اِ۬لْمَدَآئِنِ حَٰشِرِينَ ﴿53﴾ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ
لَشِرْذِمَةٞ قَلِيلُونَ ﴿54﴾ وَإِنَّهُمْ لَنَا لَغَآئِظُونَ ﴿55﴾ وَإِنَّا لَجَمِيعٌ حَذِرُونَ ﴿56﴾
فَأَخْرَجْنَٰهُم مِّن جَنَّٰتٖ وَعُيُونٖ ﴿57﴾ وَكُنُوزٖ وَمَقَامٖ كَرِيمٖ ﴿58﴾
كَذَٰلِكَ وَأَوْرَثْنَٰهَا بَنِے إِسْرَآءِيلَ ﴿59﴾ فَأَتْبَعُوهُم مُّشْرِقِينَ ﴿60﴾

ربع

39. Saboda kaunar mu bi matsafa in sun kasance sune masu rinjaye, (saboda su zarce kan addinin su baza subi Annabi Musa ba".
40. To yayin da matsafa sukazo sai sukace da Fir'auna, "Shin akwai lada garemu in mun kasnce mune masu rinjaye?"
41. Yace, "Sosai, kuma ku kuna cikin ababen kusantawa a yayin".
42. Sai Annabi Musa (Alaihissalamu) yace musu (bayan sunce "Imma ka jefa ko mu mu jefa") "Ku jefa abinda zaku jefa".
43. Sai suka jefa iggwansu da sandunansu Sukace, "Da buwayar Fir'auna lalle mune masu rinjaye".
44. Sai Annabi Musa (Alaihissalam) ya jefa sandarsa sai ga ta tana c accafke abinda suke maguđi dashi (suna nuna igiyoyin da sandunansu, cewa ita macizai ne dasuke yawo.
45. Aka yada matsafa suna masu sujada ga Allah.
46. Sukace, "Mun bada gaskiya da Ubangijin talikai.
47. "Ubangijin Annabi Musa (Alaihissalam) da Haruna (Alaihissalam,) saboda abinda suka gani na sanda bazai yiwu takan tsafi ba".)
48. Sai Fir'auna yace, "Bada gaskiya zakuyi ga Annabi Musa tun ban yi muku izini ba. Ashe shine babban ku wanda ya sanar daku ,tsafin, (yasanar daku ,wani abu nasa ya rinjaye kuda wani tsafin?) To da sannu zaku san abinda zai same ku daga gareni?.
49. "To wallahi zan yanyanke hannayenkuda kafafuwan ku a sabe, (wato hannun kowane daya ta dama da kafarsa ta hagun,) lalle zan tsistsire ku baki daya".
50. Sukace, "Ba komai a gare mu, haƙiƙa mu masu komawa ne izuwa Ubangijinmu, (bayan mutuwarmu da kowace fuska).
51. " Haƙiƙa mu muna kaunar Ubangijimnu ya gafarta mana kurakuranmu don mun kasance farkon muminai (a zamaninmu)"
52. Muka aiko izuwa Annabi Musa (Alaihissalamu bayan shekaru talatin dayayi yana kiran su izuwa Allah ta'ala da ayoyi). "Tafi da bayina Bani-Isra'ila da daddare izuwa kogi, haƙiƙa ku ababan bi ne (Fir'auna da rundunarsa zasu bi ku, muka tserar daku ,muka nutsar dasu").
53. Sai Fir'auna ya aika masu da tattaro mayaƙa a cikin garuruwa (yayin da aka bashi labari da tafiya tasu, Ance yana da birni dubu garuruwa goma sha biyu).
54. (Yana mai cewa) haƙiƙa wađannan tawaga ce kađan (an'ce dubu dari shida da dubu saba'in, 'yan kan gabana yakin dubu dad bakwai, ya karanta su saboda duba izuwa rundunar yakinsa).
55. " Haƙiƙa su masu fusatar da mune
56. "Kuma lalle mu runduna ne shiryayyu"
57. Sai muka fitar da Fir'auna da mutanensa daga (Misra, donsu riski Musa da mutanensa,) daga gonakai (data kasance a gefe biyu na Nil,) da idonduna na ruwa masu kwarara (a gidaddaji na Nil).
58. Da taskokin (dukiya na zinariya da azurfa, an ambace ta kunuzu saboda ba a fitar da hakkin Allah daga cikin ta ba,) kuma aka fishshe su daga mukami mai girma (na sarakuna da waziran su da mabiyansu suke kewaye su,
59. Kamar fitarwar mu ga wađannan mutane muka gadad da Bani-Isra'ila ita (bayan nutsar da Fir'auna da mutanensa,)
60. Sai suka dske su lokacin hudowar rana.

فَلَمَّا تَرَٰٓءَا ٱلْجَمْعَانِ قَالَ أَصْحَٰبُ مُوسَىٰٓ إِنَّا لَمُدْرَكُونَ ﴿61﴾ قَالَ كَلَّآ
إِنَّ مَعِىَ رَبِّى سَيَهْدِينِ ﴿62﴾ فَأَوْحَيْنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ أَنِ ٱضْرِب بِّعَصَاكَ
ٱلْبَحْرَ فَٱنفَلَقَ فَكَانَ كُلُّ فِرْقٍ كَٱلطَّوْدِ ٱلْعَظِيمِ ﴿63﴾ وَأَزْلَفْنَا ثَمَّ
ٱلْـَٔاخَرِينَ ﴿64﴾ وَأَنجَيْنَا مُوسَىٰ وَمَن مَّعَهُۥٓ أَجْمَعِينَ ﴿65﴾ ثُمَّ أَغْرَقْنَا
ٱلْـَٔاخَرِينَ ﴿66﴾ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَةً وَمَا كَانَ أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿67﴾
وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿68﴾ وَٱتْلُ عَلَيْهِمْ نَبَأَ إِبْرَٰهِيمَ ﴿69﴾
إِذْ قَالَ لِأَبِيهِ وَقَوْمِهِۦ مَا تَعْبُدُونَ ﴿70﴾ قَالُوا۟ نَعْبُدُ أَصْنَامًا
فَنَظَلُّ لَهَا عَٰكِفِينَ ﴿71﴾ قَالَ هَلْ يَسْمَعُونَكُمْ إِذْ تَدْعُونَ ﴿72﴾
أَوْ يَنفَعُونَكُمْ أَوْ يَضُرُّونَ ﴿73﴾ قَالُوا۟ بَلْ وَجَدْنَآ ءَابَآءَنَا
كَذَٰلِكَ يَفْعَلُونَ ﴿74﴾ قَالَ أَفَرَءَيْتُم مَّا كُنتُمْ تَعْبُدُونَ ﴿75﴾
أَنتُمْ وَءَابَآؤُكُمُ ٱلْأَقْدَمُونَ ﴿76﴾ فَإِنَّهُمْ عَدُوٌّ لِّىٓ
إِلَّا رَبَّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿77﴾ ٱلَّذِى خَلَقَنِى فَهُوَ يَهْدِينِ ﴿78﴾ وَٱلَّذِى
هُوَ يُطْعِمُنِى وَيَسْقِينِ ﴿79﴾ وَإِذَا مَرِضْتُ فَهُوَ يَشْفِينِ ﴿80﴾ وَٱلَّذِى
يُمِيتُنِى ثُمَّ يُحْيِينِ ﴿81﴾ وَٱلَّذِىٓ أَطْمَعُ أَن يَغْفِرَ لِى خَطِيٓـَٔتِى يَوْمَ
ٱلدِّينِ ﴿82﴾ رَبِّ هَبْ لِى حُكْمًا وَأَلْحِقْنِى بِٱلصَّٰلِحِينَ ﴿83﴾

ثمن

61. To, a yayin da tawagar guda biyu suka ga juna, sai abokan Annabi Musa (Alaihissalamu) Sukace, " Haƙiƙa za a riske mu (mutanen Fir'auna zasu riske mu, bamu da iko dasu).
62. Sai Annabi Musa Alaihissalam yace, (A'a, bazasu riske mu ba,) Haƙiƙa Ubangijina yana taredani (da nasararsa,) da sannu zai shirye ni (hanyar tsira").
63. Sai muka aiko izuwa Annabi Musa (Alaihissalamu) "Doki kogi da sandar ka" (saiya doke shi) saiya dare gida goma sha biyu, kowane gidaya kasance kamar dutse babba, (ga hanyoyi da suka shige ta, siddin mai doki bai yi danshi ba, ko labbatin sa).
64. Muka kusanta mutanen Fir'auna a canenka (har suka shiga hanyoyin nasu).
65. Muka tserar da Annabi Musa (Alaihissalam) da mutanensa bakiɗaya (da fishshe su daga kogi a bisa kamar su abin ambato yadda yake bai hade ba).
66. Sannan muka nutsar da sauran (Fir'auna da mutanensa shine kogin ya kife kansu, yayin da suka gama shiga cikin kogi da ficewar Bani-Isra'ila daga kogin).
67. Haƙiƙa akwai aya (izna ga waɗanda zasu wa'azantu a cikin nutsar da Fir'auna da mutanensa,) yawaicin su basu kasance masu bada gaskiya da Allah ba, (ba wanda ya bada gaskiya daga cikin su sai Asiyatu matar Fir'auna, Allah ya kara yarda gare tada Hizƙilu da Maryamu yar namusa).
68. Haƙiƙa Ubangijinka lalle shine mabuwayi (ya nutsar da kafirai,) mai jinkan muminai (ya tserar dasu daga nutsewa).

(ƘISSAR ANNABI IBRAHIMU ALAIHISSALAMU) WACCE TA ƘUNSHI ZUZZURFAN LADABI A CIKIN GA NAWA DA ALLAH.

69. Karanta wa kafiran Makka labarin Annabi Ibrahimu (alaihissalamu)
70. Yayin dayace da babansa da mutanensa, "Me kuke bautawa, to me ye haƙiƙar sa?"
71. Sukace, "Muna bautawa gumaka mu wuni muna masu dukufa a kan bautar ta", (sun kara wannan jumla don fariya da bautar gumaka).
72. Yace, "Shin suna jin ku yayin da kuke kiran su?
73. "Ko suna amfanin ku (in kun bauta musu) ko suna cutarku (in baku bauta musu) ba?")
74. Sai Sukace, ("Bako daya,) mudai mun samu iyayenmu hakana suke aikatawa".
75. Yace, "Shin ba kwa ganin abinda kuke bautawa din nan?
76. Kuda iyayen ku na da can.
77. "To haƙiƙa su magauta ne gare ni, ni bana bauta musu sai Ubangijin talikai (ni ina bauta masa).
78. "Wanda ya halicce ni to shine mai shiryar dani (izuwa addini).
79. "Wandashine yake ci dani kuma yake sha da ni".
80. "Idan nayi rashin lafiya shine yake warkar dani.
81. "Wanda shine yake karbar raina yake raya ni".
82. "Wanda nake kaunar ya gafarta min kuskurena ranar Lahira.
83. "Ya Ubangiji ka bani ilimi ka riskar dani da Annabawa.

وَاجْعَل لِّي لِسَانَ صِدْقٍ فِي الْآخِرِينَ ﴿84﴾ وَاجْعَلْنِي مِن وَرَثَةِ جَنَّةِ
النَّعِيمِ ﴿85﴾ وَاغْفِرْ لِأَبِي إِنَّهُ كَانَ مِنَ الضَّالِّينَ ﴿86﴾ وَلَا تُخْزِنِي
يَوْمَ يُبْعَثُونَ ﴿87﴾ يَوْمَ لَا يَنفَعُ مَالٌ وَلَا بَنُونَ ﴿88﴾ إِلَّا مَنْ أَتَى اللَّهَ
بِقَلْبٍ سَلِيمٍ ﴿89﴾ وَأُزْلِفَتِ الْجَنَّةُ لِلْمُتَّقِينَ ﴿90﴾ وَبُرِّزَتِ الْجَحِيمُ
لِلْغَاوِينَ ﴿91﴾ وَقِيلَ لَهُمْ أَيْنَ مَا كُنتُمْ تَعْبُدُونَ ﴿92﴾ مِن دُونِ اللَّهِ
هَلْ يَنصُرُونَكُمْ أَوْ يَنتَصِرُونَ ﴿93﴾ فَكُبْكِبُوا فِيهَا هُمْ وَالْغَاوُونَ ﴿94﴾
وَجُنُودُ إِبْلِيسَ أَجْمَعُونَ ﴿95﴾ قَالُوا وَهُمْ فِيهَا يَخْتَصِمُونَ ﴿96﴾
تَاللَّهِ إِن كُنَّا لَفِي ضَلَالٍ مُّبِينٍ ﴿97﴾ إِذْ نُسَوِّيكُم بِرَبِّ الْعَالَمِينَ ﴿98﴾
وَمَا أَضَلَّنَا إِلَّا الْمُجْرِمُونَ ﴿99﴾ فَمَا لَنَا مِن شَافِعِينَ ﴿100﴾ وَلَا صَدِيقٍ حَمِيمٍ ﴿101﴾
فَلَوْ أَنَّ لَنَا كَرَّةً فَنَكُونَ مِنَ الْمُؤْمِنِينَ ﴿102﴾ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَآيَةً
وَمَا كَانَ أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿103﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ الْعَزِيزُ الرَّحِيمُ ﴿104﴾
كَذَّبَتْ قَوْمُ نُوحٍ الْمُرْسَلِينَ ﴿105﴾ إِذْ قَالَ لَهُمْ أَخُوهُمْ نُوحٌ أَلَا تَتَّقُونَ ﴿106﴾
إِنِّي لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿107﴾ فَاتَّقُوا اللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿108﴾ وَمَا أَسْأَلُكُمْ
عَلَيْهِ مِنْ أَجْرٍ إِنْ أَجْرِيَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ الْعَالَمِينَ ﴿109﴾ فَاتَّقُوا اللَّهَ
وَأَطِيعُونِ ﴿110﴾ ۞ قَالُوا أَنُؤْمِنُ لَكَ وَاتَّبَعَكَ الْأَرْذَلُونَ ﴿111﴾

حزب

84. "Ka samui harshen gaskiya da kyakkyawan yabo a cikin mutanen karshe wanda zasu zo bayana izuwa ranar alƙiyama ".
85. "Ka sanya ni daga magadan aljannar ni'ima wato (cikin waɗanda ake basu ita).
86. "Kayi gafara ga babana, haƙiƙa shiya kasance ba a cikin shiryayyu ba (shine ka karbi tubansa kayi masa gafara. Wannan tun gaban bai fahimci cewa shi ba Musulmi ne ba, tamfar daka ambata cikin Suratu Bara'a.)
87. "Kadaka kunyatar dani ranar da ake tashin mutane".
88. Sai Ubangiji yace, A cikin ranar ALƙyama ranar da dukiyako 'ya'yabasa amfanin kowa.
89. Sai wanda yazowa Ubangiji da zuciya sumul (daga shirka da nufaka, shine zuciyar mumini, to shi mumini wannan zai amfane ,shi).
90. Aka kusanto aljanna ga masu jin tsoron Allah (saisu ganta)
91. Aka fitar da jahannama ga kafirai.
92. Aka ce dasu "Ina abinda kuka kasance kuna bautawa?
93. "Ba Allah ba (na gumaka, suna taimakon ku ga ije azaba ga barin ku) ko kuma suna taimakon junan su?
94. Sai aka kifa su a cikin ta su da halakakku,
95. Da rundunar iblis baki daya.
96. Sukace (su batattun nan) alhali suna cikin wuta suna husuma (tareda ababen bautawar nasu).
97. (Sukace,) "Abin mana ki, lamarin lalle mun kasance cikin ɓata mabayyani.
98. "Tun da muke daidaita kuda Ubangijin talikai (a cildn ibada).
99. "Ba abinda ya ɓatar da mu (ga barin shirya) sai shaidanu (ko na farkon mu waɗanda mukayi koyi dasu).
100. "To bamu da masu ceto (kamar yadda muminai suke dashi na daga Annabawa da Mala'ikuda muniinai) ba aboki mai kulawa (garemu).
101. Da ma akwai komowa garemu (izuwa duniya,) mu kasance cikin muminai?
102. Haƙiƙa akwai aya cikin wancananka abin (ambato na ƙissar Annabi Ibrahimu alaihissalamu da mutanensa,) yawancin su basu kasance muminai ba.
103. Haƙiƙa Ubangijinka lalle shine mabuwayi mai rahama.

(ƘISSAR ANNABI NUHU ALAIHISSALAMU) DA ABINDA TA KUNSA NA DAGA RAUNANAN MABIYANSA, DA KULAWAR SA DASU.

104. Mutanen Annabi Nuhu (Alaihissalamu) sun ƙaryata manzanin (saboda sunyi tarayya dashi a tsawon zaman sa a cikin su, ya zama kamar manzanni.
105. Yayin da dan uwansu a nasaba yace dasu "Shin ba kwaji tsoron Allah ba?"
106. " Haƙiƙa ni manzo ne amintacce (bisa iyar da aike).
107. "Kuji tsoron Allah ku bini (a cikin abinda nake umarnin ku dashi na kadaita Allah).
108. "Ni ban tambaye ku lada bisa ida aike ba, ni ladana yana gurin Ubangijin talikai.
109. Sai kuji tsoron Allah kubini (ya maimaita wannan saboda takidi")
110. Sukace, "Yaya zamu bada gaskiya dakai (don maganarka,) ga kananan mutane mafi kaskasci sune suke bin ka, (masaka, da masu goge takalma da masu dinka su").
111. (Sai yace,) "Ni bani da sani cikin abinda suke aikatawa.

قَالَ وَمَا عِلْمِي بِمَا كَانُواْ يَعْمَلُونَ ﴿112﴾ إِنْ حِسَابُهُمْ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّي
لَوْ تَشْعُرُونَ ﴿113﴾ وَمَا أَنَا بِطَارِدِ الْمُؤْمِنِينَ ﴿114﴾ إِنْ أَنَا إِلَّا نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿115﴾
قَالُواْ لَئِن لَّمْ تَنتَهِ يَٰنُوحُ لَتَكُونَنَّ مِنَ الْمَرْجُومِينَ ﴿116﴾ قَالَ رَبِّ
إِنَّ قَوْمِي كَذَّبُونِ ﴿117﴾ فَافْتَحْ بَيْنِي وَبَيْنَهُمْ فَتْحًا وَنَجِّنِي وَمَن
مَّعِيَ مِنَ الْمُؤْمِنِينَ ﴿118﴾ فَأَنجَيْنَٰهُ وَمَن مَّعَهُ فِي الْفُلْكِ الْمَشْحُونِ ﴿119﴾
ثُمَّ أَغْرَقْنَا بَعْدُ الْبَاقِينَ ﴿120﴾ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَءَايَةً وَمَا كَانَ
أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿121﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ الْعَزِيزُ الرَّحِيمُ ﴿122﴾
كَذَّبَتْ عَادٌ الْمُرْسَلِينَ ﴿123﴾ إِذْ قَالَ لَهُمْ أَخُوهُمْ هُودٌ أَلَا تَتَّقُونَ ﴿124﴾
إِنِّي لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿125﴾ فَاتَّقُواْ اللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿126﴾ وَمَا أَسْـَٔلُكُمْ
عَلَيْهِ مِنْ أَجْرٍ إِنْ أَجْرِيَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ الْعَٰلَمِينَ ﴿127﴾ أَتَبْنُونَ بِكُلِّ رِيعٍ
ءَايَةً تَعْبَثُونَ ﴿128﴾ وَتَتَّخِذُونَ مَصَانِعَ لَعَلَّكُمْ تَخْلُدُونَ ﴿129﴾
وَإِذَا بَطَشْتُم بَطَشْتُمْ جَبَّارِينَ ﴿130﴾ فَاتَّقُواْ اللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿131﴾ وَاتَّقُواْ
الَّذِي أَمَدَّكُم بِمَا تَعْلَمُونَ ﴿132﴾ أَمَدَّكُم بِأَنْعَٰمٍ وَبَنِينَ ﴿133﴾ وَجَنَّٰتٍ
وَعُيُونٍ ﴿134﴾ إِنِّي أَخَافُ عَلَيْكُمْ عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿135﴾
قَالُواْ سَوَآءٌ عَلَيْنَا أَوَعَظْتَ أَمْ لَمْ تَكُن مِّنَ الْوَٰعِظِينَ ﴿136﴾

112. "Sakamakon su bai kasance basai gurin Ubangijina, da kun san (haka da baku laifanta su ba).
113. "Ni ba mai kore muminai ne ba.
114. "Ni mai gargadI ne mabayyanin gargadi".
115. Sukace, "Wallahi Ya Nuhu (alaihissalamu) in baka hanu ga barin abinda kake fada ba, zaka kasance cikin ababan jejjefewa (da duwatsu ko zagi)".
116. Annabi Nuhu yace, "Ubangijina, hakika mutanena sun karyatani!
117. "Kayi hukunci tsakanina da tsakaninsu ka tserar dani da wadanda suke taredani na daga muminai".
118. (Ubangiji yace,) "Sai muka tserar dashi da wadanda suke tare dashi cikin jirgi abin cikawa (da talikai).
119. "Sannan muka nutsar da ragowar (mutanensa bayan wadanda aka tserar dasu").
120. Hakika aikin wancanenka akwai aya, yawaicinsu basu kasance muminai ba.
121. Hakika Ubangijinka lalle shine mabuwayi mai jinkai.

(KISSAR ANNABI HUDU ALAIHISSALAMU)DA ABINDA TAKUNSA NA GINE - GINEN HASUMIYOYI, DATANKUNAN RUWA, AKARKASHIN KASA. DA KEMASAR ZUCIYA WANDAYA AFKU DAGA MUTANENSA. DA SAKAMAKO DA ISKA MAIAMO DA AKARARAKA A KANSU)

122. Adu sun karyata manzanni.
123. Zamanin da dan uwansu a nasaba yace dasu "Shin ba kwaji tsoron Ubangiji ba? (Ma'ana kuji tsoron Ubangiji).
124. " Hakika.ni jakada ne izuwa gareku amintacce.
125. Kuji tsoron Allah kubi ni
126. Ban tambaye ku lada bisa ida aike ba ladana bai kasance ba sai ga Ubangijin talikai.
127. Donme kuke ginawar gini a kowane tudu don alama ga masu wucewa kuna wasa (da wanda ya wuce ku).
128. "Kuna rikon taffukka karkashin ruwa kamar zaku dauwama (a kan kasa bazaku mutu ba).
129. "In zakuyi danka (da duka ko kisa) kuna danka ta jabberai (bada jinkai ba).
130. Ku tsoraci Allah (a cikin wancananka) kubini (cikin abinda nake umarnin ku dashi).
131. "Kuji tsoron wanda ya kare kuda abinda kuka sani".
132. Ya ni'imta kuda dabbobi da bisashe da 'ya'yaye.
133. Da gonaki da koramu.
134. Ni ina jin tsoron azabar rana mai girma a gareku (a duniya da Lahira in kuka sabe ni).
135. Sukace, "Daidai ne gare mu, kayi wa'azi ko bakasance cikin masu wa'azi ba bazamu daddara saboda wa'azin ka ba.
136. Abinda kake mana wa'azi dashi bai kasance ba saitadar mutanen farko.

إِنْ هَٰذَا إِلَّا خُلُقُ الْأَوَّلِينَ ﴿137﴾ وَمَا نَحْنُ بِمُعَذَّبِينَ ﴿138﴾
فَكَذَّبُوهُ فَأَهْلَكْنَاهُمْ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَآيَةً وَمَا كَانَ
أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿139﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ الْعَزِيزُ الرَّحِيمُ ﴿140﴾
كَذَّبَتْ ثَمُودُ الْمُرْسَلِينَ ﴿141﴾ إِذْ قَالَ لَهُمْ أَخُوهُمْ صَالِحٌ أَلَا تَتَّقُونَ ﴿142﴾
إِنِّي لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿143﴾ فَاتَّقُوا اللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿144﴾ وَمَا أَسْأَلُكُمْ
عَلَيْهِ مِنْ أَجْرٍ إِنْ أَجْرِيَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ الْعَالَمِينَ ﴿145﴾ * أَتُتْرَكُونَ ثمن
فِي مَا هَاهُنَا آمِنِينَ ﴿146﴾ فِي جَنَّاتٍ وَعُيُونٍ ﴿147﴾ وَزُرُوعٍ وَنَخْلٍ طَلْعُهَا
هَضِيمٌ ﴿148﴾ وَتَنْحِتُونَ مِنَ الْجِبَالِ بُيُوتًا فَرِهِينَ ﴿149﴾ فَاتَّقُوا اللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿150﴾
وَلَا تُطِيعُوا أَمْرَ الْمُسْرِفِينَ ﴿151﴾ الَّذِينَ يُفْسِدُونَ فِي الْأَرْضِ وَلَا يُصْلِحُونَ ﴿152﴾
قَالُوا إِنَّمَا أَنتَ مِنَ الْمُسَحَّرِينَ ﴿153﴾ مَا أَنتَ إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُنَا
فَأْتِ بِآيَةٍ إِن كُنتَ مِنَ الصَّادِقِينَ ﴿154﴾ قَالَ هَٰذِهِ نَاقَةٌ لَّهَا
شِرْبٌ وَلَكُمْ شِرْبُ يَوْمٍ مَّعْلُومٍ ﴿155﴾ وَلَا تَمَسُّوهَا بِسُوءٍ
فَيَأْخُذَكُمْ عَذَابُ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿156﴾ فَعَقَرُوهَا فَأَصْبَحُوا
نَادِمِينَ ﴿157﴾ فَأَخَذَهُمُ الْعَذَابُ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَآيَةً وَمَا كَانَ
أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿158﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ الْعَزِيزُ الرَّحِيمُ ﴿159﴾

137. Mu ba ababan yi wa azaba ne ba.
138. Sai suka ƙaryata shi, sai muka halaka su (a duniya da iska)[1] haƙiƙa a cikin wancananka akwai aya, yawaicinsu basu kasance muminai ba.
139. Haƙiƙa Ubangijinka lalle shine mabuwayi mai jinkai.

(ƘISSAR ANNABI SALIHU ALAIHISSALAMU)

140. Samudu sun ƙaryata manzanni.
141. Yayin da dan uwansu (a kabila) yace dasu "Shin ba kwa ji tsoron Allah ba, (ma'ana kuji tsoron Allah).
142. " Haƙiƙa ni manzo ne a gareku amintacce.
143. Kuji tsoron Allah kubi ni
144. Ni ban tambaye ku lada bisa ida aike ba, ladana bai ƙasance ba sai gurin Ubangijin talikai.
145. Yanzu a bar ku a cikin abinda yake wannan guri (na alheri) kuna amintattu.
146. Cikin gonakai da idanduna.
147. Da hatsaitsaida dabinai, hudar ta mai laushi.
148. "Kuna sassakawan dakuna da duwarwatsai kuna masu butulci ga Allah.
149. "To kuji tsoron Allah kubini (cikin abinda na umarce ku dashi)".
150. "Kadaku ,bi umarnin masu barna".
151. Waɗanda suke barna a cikin ƙasa basuna gyara ba,
152. Suka ee, "Dahir kai kana cikin kan ababen rinjaye kan hankalinsu".
153. kai ba komai ne ba illa mutum tamkar mu.
154. Ka zoda ayain ka kasance cikin masu gaskiya (a jakadancin ka).

(TSORATARWA DAGA CUTAR NAKATUSALIHI ALAIHISSALAM DA MAKAMANCINSA KAMAR AHLU-BAITI RASULULLAHI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA DA WALIYYAN ALLAH YARDAR ALLAH TA DAUWAMA A GARESU)

155. Yace, "Wannan taguwa ce, rabo (na ruwa) na gare ta, ku kuma kuna da rabo (na ruwa) a rana abar sani.
156. "Kadaku ,shafe tada mugu sai azabar rana mai girma ta shafe ku".
157. Suka sare ta (wato Kudaru ya sare ta dayardarsu) sai suka zamamasu nadama (a bisasare ta).
158. Sai azabata rike su (a wannan rana suka halaka a cikin wancananka). Haƙiƙa akwai aya a cikin wancananka, yawancinsu ba muminai ba ne.
159. Haƙiƙa Ubangijinka lalle shine mabuwayi mai rahama.

1) Yawancin su basu kasance muminai ba sai kadan, sun kasance tareda Annabi Hudu Alaihissalamu, sai iska mai laushi tana sabas su har wancananka muddata wuce ma kwana bakwai da wuni takwas, sai Yakura daga wurin su zuwa Makka, Ance kabarinsa yana gurin dawafi, kuma, ance yana ƙasar Dimashƙa. -Sanajiy -

كَذَّبَتْ قَوْمُ لُوطٍ الْمُرْسَلِينَ ﴿١٦٠﴾ إِذْ قَالَ لَهُمْ أَخُوهُمْ لُوطٌ أَلَا تَتَّقُونَ ﴿١٦١﴾
إِنِّي لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿١٦٢﴾ فَاتَّقُوا اللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿١٦٣﴾ وَمَا أَسْأَلُكُمْ
عَلَيْهِ مِنْ أَجْرٍ إِنْ أَجْرِيَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ الْعَالَمِينَ ﴿١٦٤﴾ أَتَأْتُونَ
الذُّكْرَانَ مِنَ الْعَالَمِينَ ﴿١٦٥﴾ وَتَذَرُونَ مَا خَلَقَ لَكُمْ رَبُّكُمْ
مِنْ أَزْوَاجِكُمْ بَلْ أَنْتُمْ قَوْمٌ عَادُونَ ﴿١٦٦﴾ قَالُوا لَئِنْ لَمْ تَنْتَهِ يَا لُوطُ
لَتَكُونَنَّ مِنَ الْمُخْرَجِينَ ﴿١٦٧﴾ قَالَ إِنِّي لِعَمَلِكُمْ مِنَ الْقَالِينَ ﴿١٦٨﴾ رَبِّ نَجِّنِي
وَأَهْلِي مِمَّا يَعْمَلُونَ ﴿١٦٩﴾ فَنَجَّيْنَاهُ وَأَهْلَهُ أَجْمَعِينَ ﴿١٧٠﴾
إِلَّا عَجُوزًا فِي الْغَابِرِينَ ﴿١٧١﴾ ثُمَّ دَمَّرْنَا الْآخَرِينَ ﴿١٧٢﴾ وَأَمْطَرْنَا
عَلَيْهِمْ مَطَرًا فَسَاءَ مَطَرُ الْمُنْذَرِينَ ﴿١٧٣﴾ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَآيَةً
وَمَا كَانَ أَكْثَرُهُمْ مُؤْمِنِينَ ﴿١٧٤﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ الْعَزِيزُ الرَّحِيمُ ﴿١٧٥﴾
كَذَّبَ أَصْحَابُ لْئَيْكَةِ الْمُرْسَلِينَ ﴿١٧٦﴾ إِذْ قَالَ لَهُمْ شُعَيْبٌ أَلَا تَتَّقُونَ ﴿١٧٧﴾
إِنِّي لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿١٧٨﴾ فَاتَّقُوا اللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿١٧٩﴾ وَمَا أَسْأَلُكُمْ
عَلَيْهِ مِنْ أَجْرٍ إِنْ أَجْرِيَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ الْعَالَمِينَ ﴿١٨٠﴾ * أَوْفُوا الْكَيْلَ
وَلَا تَكُونُوا مِنَ الْمُخْسِرِينَ ﴿١٨١﴾ وَزِنُوا بِالْقِسْطَاسِ الْمُسْتَقِيمِ ﴿١٨٢﴾
وَلَا تَبْخَسُوا النَّاسَ أَشْيَاءَهُمْ وَلَا تَعْثَوْا فِي الْأَرْضِ مُفْسِدِينَ ﴿١٨٣﴾

ربع

(ƘISSAR ANNABI LUƊU DA MUTANENSA ALAIHISSALATU WASSALAMU)

160. Mutanen Annabi Luɗu (alaihissalamu) sun ƙaryata manzanni,
161. Lokacin da ɗan uwansu (a zaman gari Annabi Luɗu yace dasu, "Shin ba kwa ji tsoron Allah ba, ma'ana ai kuji tsoron Allah.
162. Haƙiƙa ni jakada ne gareku amintacce.
163. Kuji tsoron Allah kubi ni.
164. Ban tambaye ku lada bisa ida aike ba ladana bai kasance ba sai a gurin ubangijin talikai.
165. "Donme kuke zowa maza na daga mutane?
166. Ku ke barin abinda Ubangijinku ya halitta don ku (shine gabanbanin matayen ku, wato farjojin su) kai ku dai mutane ne masu shisshigi".
167. Sukace, "Wallahi Ya Luɗu in baka hanu (ga barin yi mana inkari ba,) lalle zaka zama cikin ababan firarwa (daga garinmu").
168. (Annabi Luɗu) yace, " Haƙiƙa ni ina cikin masu ki ga aikin ku.
169. "Ubangijina tserar dani da iyalina daga abinda suke aikatawa (watau daga azabarsa").
170. Muka tserar dashi da iyalinsa baki daya.
171. Sai wata gyatuma (mata tasa) cikin masu wanzuwa (muka halakar da ita).
172. Sannan muka rugurguje sauran.
173. Muka saukar da ruwa na duwarwatsu a kansu na daga halakarwar sai ruwan ababan baiwa tsoro ya mugusta.
174. Haƙiƙa a cikin wancananka lalle akwai aya, yawaicin su basu kasance muminai ba.
175. Haƙiƙa Ubangijinka lalle shine mabuwayi (Ya halakar da kafirai dukkan su) mai jinƙai (yajiƙan muminai dukkan su.)

(ƘISSAR ANNABI SHITAIBU ALAIHISSALAMU)

176. Mutanen Runƙunƙa (wato gandun daji na giginya) sun karyata manzanni.
177. Zamanin da Annabi Shu'aibu (alaihissalamu) yace dasu, "Shin ba kwa tsoraci Ubangiji ba? (Bai ce ɗan uwansu ba saboda ba nasaba tsakaninsu, ma'ana kuji tsoron Allah)
178. "Ni jakadan Allah ne izuwa gareku amintacce".
179. kuji tsoron Allah kubi ni.
180. Bana tambayon ku lada bisa ida aike, ladana bai kasance ba sai ga Ubangijin talikai.
181. Ku cika mudu ka daku ,kasance daga masu tauyewa.
182. Ku auna da ma'auni madaidaici
183. Kadaku ,tauye wa mutane kayayyakinsu (kadaku ,tauye komai na hakkinsu,) kada kuyi ɓarna a bayan ƙasa kuna mabarnata (da kisa da waninsa)".

وَاتَّقُوا الَّذِي خَلَقَكُمْ وَالْجِبِلَّةَ الْأَوَّلِينَ ﴿١٨٤﴾ قَالُوا إِنَّمَا أَنتَ مِنَ
الْمُسَحَّرِينَ ﴿١٨٥﴾ وَمَا أَنتَ إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُنَا وَإِن نَّظُنُّكَ لَمِنَ الْكَاذِبِينَ ﴿١٨٦﴾
فَأَسْقِطْ عَلَيْنَا كِسَفًا مِّنَ السَّمَاءِ إِن كُنتَ مِنَ الصَّادِقِينَ ﴿١٨٧﴾
قَالَ رَبِّي أَعْلَمُ بِمَا تَعْمَلُونَ ﴿١٨٨﴾ فَكَذَّبُوهُ فَأَخَذَهُمْ عَذَابُ
يَوْمِ الظُّلَّةِ إِنَّهُ كَانَ عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿١٨٩﴾ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَآيَةً
وَمَا كَانَ أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿١٩٠﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ الْعَزِيزُ الرَّحِيمُ ﴿١٩١﴾
وَإِنَّهُ لَتَنزِيلُ رَبِّ الْعَالَمِينَ ﴿١٩٢﴾ نَزَلَ بِهِ الرُّوحُ الْأَمِينُ ﴿١٩٣﴾
عَلَىٰ قَلْبِكَ لِتَكُونَ مِنَ الْمُنذِرِينَ ﴿١٩٤﴾ بِلِسَانٍ عَرَبِيٍّ مُّبِينٍ ﴿١٩٥﴾
وَإِنَّهُ لَفِي زُبُرِ الْأَوَّلِينَ ﴿١٩٦﴾ أَوَلَمْ يَكُن لَّهُمْ آيَةً أَن يَعْلَمَهُ عُلَمَاءُ
بَنِي إِسْرَائِيلَ ﴿١٩٧﴾ وَلَوْ نَزَّلْنَاهُ عَلَىٰ بَعْضِ الْأَعْجَمِينَ ﴿١٩٨﴾ فَقَرَأَهُ
عَلَيْهِم مَّا كَانُوا بِهِ مُؤْمِنِينَ ﴿١٩٩﴾ كَذَٰلِكَ سَلَكْنَاهُ فِي قُلُوبِ
الْمُجْرِمِينَ ﴿٢٠٠﴾ لَا يُؤْمِنُونَ بِهِ حَتَّىٰ يَرَوُا الْعَذَابَ الْأَلِيمَ ﴿٢٠١﴾
فَيَأْتِيَهُم بَغْتَةً وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿٢٠٢﴾ فَيَقُولُوا هَلْ نَحْنُ
مُنظَرُونَ ﴿٢٠٣﴾ أَفَبِعَذَابِنَا يَسْتَعْجِلُونَ ﴿٢٠٤﴾ أَفَرَأَيْتَ إِن
مَّتَّعْنَاهُمْ سِنِينَ ﴿٢٠٥﴾ ثُمَّ جَاءَهُم مَّا كَانُوا يُوعَدُونَ ﴿٢٠٦﴾

184. Kuji tsoron Allah wanda ya halicce ku ya halicci mutanen farko.
185. Sukace, "Kai haƙiƙa kana cikin ababan rinjaye a kan hankalinsu".
186. "Kai ba komai bane sai mutumirinmu, shi lamarin lalle muna zaton ka kana cikin marasa gaskiya".
187. "Ka saryo dayanki a kanmu daga sama in ka kasance cikin magaskata (a cikin aiken ka").
188. Yace, "Ubangijina ne masani da abindaku ,ke aikatawa (zaiyi muku sakamako a kansa".)
189. Sai suka ƙaryarta shi, sai azabar ranar girgizanya ta sauka a kansu (azabar girgije data sauka a kansu bayan zafi mai tsanani daya same su, saita kwararo wuta a kansu, suka ƙone , suka zamo toka. sun yi wa kansu tayani haka, saboda sun nemi kisfowar sama a kansu saiya same sun.) Haƙiƙa wannan azaba ta kasance azaba mai girma.
190. Haƙiƙa lalle akwai aya cikin wancananka, yawaicin su basu kasance muminai ba.
191. Haƙiƙa Ubangijinka lalle shine mabuwayi (a kan kafirai gaba daya) mai jinkai ga (muminai gaba daya).

(KIRARI GA ALƘUR'ANI DA MATSAYIN SA GURIN MUSHURIKAI)

192. Haƙiƙa shi Alƙur'ani lalle saukarwar Ubangijin talikai ne.
193. Mala'ika Jibrilu ne ya saukar dashi.
194. A bisa zuciyarka donka kasance cikin masu gargaɗi.
195. Da harshe Balarabe mabayyani. ba gargaliyya ba.
196. Haƙiƙa shi (Alƙur'ani abin saukarwa bisa Annabi Sallallahu alaihi wasallama), lalle yana cikin (littattafan) farko (kamar Attaura da Injila).
197. Cewa malanan Bani-Isra'ila sunsanshi bai kasance aya a kan wancananka ga kafiran Makka ba (kamar Abdullahi Ibn Salamu da abokansa) da waɗanda suka bada gaskiya dashi, Haƙiƙa su suna bada labari da wancananka).
198. Da mun saukar dashi a bisa ba'alin bebayi,
199. Ya karanta shi a garesu bazasu zama masu bada gaskiya dashi ba.
200. Kamar shigarwarmu wancananka karyatawa saboda dakaratun baubawa, muka shigar da karyatawar su masu laifi (kafiran Makka saboda karatun Annabi Sallallahu alaihi wasallama).
201. Bazasu bada gaskiya dashi ba sai sun ga azaba mai raɗaɗi,
202. Tazo musu badashiri ba alhali su basu sani ba!
203. Saisu ce, "Shin yanzu a mu saurara mana (don mu bada gaskiya? Sai a ce dasu a'a, sukace yaushe ne wannan azaba?)
204. (Sai Ubangiji yace,) "Shin to da azabarmu ne suke gaggawa?"
205. Bani labari in na jiyar dasu daɗi shekaru.
206. Sannan abinda ake yi musu alwashi dashi (na azaba) yazo musu.

ثمن

مَآ أَغْنَىٰ عَنْهُم مَّا كَانُواْ يُمَتَّعُونَ ﴿207﴾ * وَمَآ أَهْلَكْنَا مِن
قَرْيَةٍ إِلَّا لَهَا مُنذِرُونَ ﴿208﴾ ذِكْرَىٰ وَمَا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ﴿209﴾
وَمَا تَنَزَّلَتْ بِهِ الشَّيَٰطِينُ ﴿210﴾ وَمَا يَنۢبَغِي لَهُمْ
وَمَا يَسْتَطِيعُونَ ﴿211﴾ إِنَّهُمْ عَنِ السَّمْعِ لَمَعْزُولُونَ ﴿212﴾
فَلَا تَدْعُ مَعَ اللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ فَتَكُونَ مِنَ الْمُعَذَّبِينَ ﴿213﴾
وَأَنذِرْ عَشِيرَتَكَ الْأَقْرَبِينَ ﴿214﴾ وَاخْفِضْ جَنَاحَكَ لِمَنِ اتَّبَعَكَ
مِنَ الْمُؤْمِنِينَ ﴿215﴾ فَإِنْ عَصَوْكَ فَقُلْ إِنِّي بَرِيٓءٌ مِّمَّا تَعْمَلُونَ ﴿216﴾
فَتَوَكَّلْ عَلَى الْعَزِيزِ الرَّحِيمِ ﴿217﴾ الَّذِي يَرَىٰكَ حِينَ تَقُومُ ﴿218﴾
وَتَقَلُّبَكَ فِي السَّٰجِدِينَ ﴿219﴾ إِنَّهُۥ هُوَ السَّمِيعُ الْعَلِيمُ ﴿220﴾
هَلْ أُنَبِّئُكُمْ عَلَىٰ مَن تَنَزَّلُ الشَّيَٰطِينُ ﴿221﴾ تَنَزَّلُ عَلَىٰ كُلِّ أَفَّاكٍ أَثِيمٍ ﴿222﴾
يُلْقُونَ السَّمْعَ وَأَكْثَرُهُمْ كَٰذِبُونَ ﴿223﴾ وَالشُّعَرَآءُ يَتَّبِعُهُمُ
الْغَاوُۥنَ ﴿224﴾ أَلَمْ تَرَ أَنَّهُمْ فِي كُلِّ وَادٍ يَهِيمُونَ ﴿225﴾ وَأَنَّهُمْ يَقُولُونَ
مَا لَا يَفْعَلُونَ ﴿226﴾ إِلَّا الَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ الصَّٰلِحَٰتِ
وَذَكَرُواْ اللَّهَ كَثِيرًا وَانتَصَرُواْ مِنۢ بَعْدِ مَا ظُلِمُواْ
وَسَيَعْلَمُ الَّذِينَ ظَلَمُوٓاْ أَيَّ مُنقَلَبٍ يَنقَلِبُونَ ﴿227﴾

207. Jiyar dasu daɗi bazai amfana musu komai ba (a cikin ije azaba).
208. Bamu halakar da wata alƙarya ba face tana da masu gargaɗi.
209. Don gargaɗi garesu, bamu kasance masu zalinci ba, acikin halakar dasu (bayan gargadin). (RADDI GA MUSHURIKAI DA HANA SATAR JI)
210. Shaiɗanu basu sauka da wannan Alƙur'ani ba.
211. Bazai kamata garesu su saukar dashi ba, bazasu sami ikon saukar dashi ba.
212. Haƙiƙa su ababan nisantawa ne ga barin jin zancen Mala'iku, (saboda ma su na taurad da ake jifan su dashi).

(NASIHOHI DAGA UBANGIJI MADAUKAKI GA MA'AIKI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA DA AL'UMARSA)

213. Kadaka bautawa wani daban abin bautawa tareda Allah sai ka kasance cikin ababan yi wa azaba, (in ka aikata abinda suke kiran ka izuwa gareshi).
214. ka gargaɗi danginka mafiYakusanci, (sune Banu-Hashim da Banul-Muɗɗalibi, yayi musu gargaɗi a sarari, Bukhari da Muslim sun ruwaito haka).
215. ka tausasa zaman tarayyar ka ga wanda yabika na daga muminai
216. Idan suka saɓe ka cene, "Ni makubuci ne daga abinda kuke aikatawa (na bautar wanin Allah").
217. Ku dogara bisa mabuwayi mai jinƙai (wato ka zuba masa dukkan al'amarin ka). (HULURI A CIKIN SALLAH DA WANINTA)
218. Wanda yake ganin ka zamanin da kake tashi (izuwa salla),
219. Da jujjuyawar ka cikin ruku'un sallah (kana tsaye ko kana zaune ko kana sunkuye ko kana mai dungura goshin ka a cikin masallata, wato cikin jama'a wacce ake sallar jam'i,)
220. Haƙiƙa Ubangiji shine mai ji mai gani, (yana jin ganawar da mai sallah yake yi dashi, yasan halin da yake ciki kamar yadda yake ba a cikin sallah ba).

(RADDI A KAN WANDA YAKE SIFFANTA ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA DA BOKAKO MAWAƘI)

221. Shin bana baku labari ba, ku kafiran Makka, a bisawa shaiɗanu suke sauka?
222. Suna sauka ne a bisa dukkan mai girba ƙarya fajiri, (kamar Musailamatu da wanin sa na bokaye).
223. Su shaiɗanu suna jefa abinda sukaji shi daga Mala'iku ga bokaye, yawaicin su makaryata ne, (wannan ya afkune tun kafin ba a tsare shaiɗanu ga barin satar ji ba). (MAWAKA MASUYI WA MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA ZAMBO)
224. Mawaka kafirai halakakku suna binsu (a cikin wakarsu su faɗeshi su ruwaitar dashi, su waɗannan ababan zargi ne (kamar Abdullahi ɗan Zubi'ira da Hubairatu ɗan Abi Wahabu Mahzumiy da Musafi'u ɗan Abdulmunafin, da Abu'izzatada Amru ɗan Abdullahi Aljumali da Umaiyatu ɗan Abi Salti Assaƙafi).
225. Shin baka sani haƙiƙa su suna nausawa a kowane zaza ba (na daga zazekun zance da reshensa).
226. Kuma suna faɗar abinda basu aikata ba (wato suna ƙarya).

(MAWAƘA ABABAN YABO)

227. sai waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki na gargaru na daga mawaka (kamar Hassanu Ibn Sabitin da Abdullahi Ibn Rawahatada Ka'abu ɗan Malikuda makamantansu na mawakan sahabbai, kamar mai wuturiyya da Hamziyya da Alfazazi da Busiri da Bura'i da Sarsari da Alkali Iyal da Ahmadu Buhlulu da Ansari da Yusifun Nabahani da makamantansu, Allah ya kara yarda garesu) suka ambaci Allah ambato mai yawa suka zambaci kafirai bayan an zalince su da zambon kafiran dasuke musu, to waɗannan ba ababan zargi ba ne. Bari Sudai ababan yabo ne!) Da sannu waɗanda sukayi zalunci (na mawaka nan da wanin su) da sannu zasu san kowace irin majuyace suke juyawa (bayan mutuwa).

27 سُورَةُ النَّمْلِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ خَمْسٌ وَتِسْعُونَ ءَايَةً 95

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

طسٓ تِلْكَ ءَايَٰتُ الْقُرْءَانِ وَكِتَابٍ مُّبِينٍ ۝1 هُدًى وَبُشْرَىٰ لِلْمُؤْمِنِينَ ۝2
الَّذِينَ يُقِيمُونَ الصَّلَوٰةَ وَيُؤْتُونَ الزَّكَوٰةَ وَهُم بِالْءَاخِرَةِ هُمْ يُوقِنُونَ ۝3
إِنَّ الَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِالْءَاخِرَةِ زَيَّنَّا لَهُمْ أَعْمَالَهُمْ فَهُمْ يَعْمَهُونَ ۝4
أُوْلَٰٓئِكَ الَّذِينَ لَهُمْ سُوٓءُ الْعَذَابِ وَهُمْ فِي الْءَاخِرَةِ هُمُ الْأَخْسَرُونَ ۝5
* وَإِنَّكَ لَتُلَقَّى الْقُرْءَانَ مِن لَّدُنْ حَكِيمٍ عَلِيمٍ ۝6 إِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِأَهْلِهِۦٓ
إِنِّيٓ ءَانَسْتُ نَارًا سَـَٔاتِيكُم مِّنْهَا بِخَبَرٍ أَوْ ءَاتِيكُم بِشِهَابٍ قَبَسٍ لَّعَلَّكُمْ تَصْطَلُونَ ۝7
فَلَمَّا جَآءَهَا نُودِيَ أَنۢ بُورِكَ مَن فِي النَّارِ وَمَنْ حَوْلَهَا وَسُبْحَٰنَ اللَّهِ رَبِّ الْعَٰلَمِينَ ۝8
يَٰمُوسَىٰٓ إِنَّهُۥٓ أَنَا اللَّهُ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ ۝9 وَأَلْقِ عَصَاكَ فَلَمَّا رَءَاهَا تَهْتَزُّ
كَأَنَّهَا جَآنٌّ وَلَّىٰ مُدْبِرًا وَلَمْ يُعَقِّبْ يَٰمُوسَىٰ لَا تَخَفْ إِنِّي لَا يَخَافُ لَدَيَّ
الْمُرْسَلُونَ ۝10 إِلَّا مَن ظَلَمَ ثُمَّ بَدَّلَ حُسْنًۢا بَعْدَ سُوٓءٍ فَإِنِّي غَفُورٌ رَّحِيمٌ ۝11
وَأَدْخِلْ يَدَكَ فِي جَيْبِكَ تَخْرُجْ بَيْضَآءَ مِنْ غَيْرِ سُوٓءٍ فِي تِسْعِ ءَايَٰتٍ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ
وَقَوْمِهِۦٓ إِنَّهُمْ كَانُواْ قَوْمًا فَٰسِقِينَ ۝12 فَلَمَّا جَآءَتْهُمْ ءَايَٰتُنَا مُبْصِرَةً قَالُواْ هَٰذَا سِحْرٌ مُّبِينٌ ۝13

رُبع

Suratun Namli

A Makka Aka. Saukar Da Ita Ayoyinta. Casa'in Da Biyar (95)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

Wannan sura ta ƙunshi ƙissoshi biyar, ƙissar Annabi Musa Alaihissalamu da kissar Annabi Dawuriu da Annabi Sulaimanu, tsiran Allah ya tabba a garesu da Alhudu- huđu da Tumruwa da Karamar Waliyyai da girman bil- Adam a kan aljan da ƙissar Annabi Salihu da Annabi Luđu, da dalilai kan wahadaniyyar Allah da ikonsa da Tashin Alƙiyama da Alƙur'ani tareda Ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wasallama, da ba'alin alamomin Alƙiyama da falalar zikiri da kira izuwa bautar Allah Sauran kuma hikimomi ne da gargade-gargade'

(TASIRIN AIḰUR'ANI A CIKIN ZUKATAN MUMINAI) DH.S

1. DH.S. (Allahu- a'lamu- bi muradihi- bizalika,) wađannan ayoyi ne na Alƙur'ani da littafi mai bayyanawar karya da gaskiya.
2. Shiriya ne (daga ɓata), albishir ne ga muminai (masu gasktawa dashi đashiga aljanna).
3. Wađanda suke tsayar da sallah (tareda hakkokin ta) suke bada zakka alhali su suna sakankancewa da ranar Lahira.
4. Haƙiƙa wađanda basu bada gaskiya da ranar Lahira ba, mun kawata musu ayyukansu (miyagu ta hanyar sha'awa har suka gan ta kyakkyawa,) to su suna dimuwa (saboda munin ta gurin mu).
5. Wađancananka mummunar azaba na garesu (a duniya kisa da ribacewa) kuma su a Lahira sune ainihin mafiya tabewa (saboda komawar su izuwa wuta abar dauwamawa a kansu).
6. Haƙiƙa kai (Annabi Sallallahu alaihi wasallama) ana saukar da ƙur'ani gareka, daga gwani mai cikakken sani (cikin wancananka).

(ḰISSAR ANNABI MUSA ALAIHISSALAMU)

7. Ka ambata ga mutanen ka zamanin da Annabi Musa yace da iyalinsa (mata tasa yayin tahowa tasa daga Madyana izuwa Misra, yace,) "Ni haƙiƙa ni na gano wuta (daga nesa,) da sannu zan zo mukuda labari (daga gare ta, alhali ya bace wa hanya,) ko in zo mukuda harshen wuta abin dosona saboda kwa ji dimi (ku ije sanyi".)
8. To, yayin dayazo mata, sai akayi kira da cewa Allah ya albarkaci wanda yake cikin wuta (shine Annabi Musa) da wanda Yake daura da ita (na Mala'iku,) Tsarki ya tabbatarwa Ubangijin talikai.
9. Ya Musa, haƙiƙa cewa lamarin, Nine Allah mabuwayi gwani.
10. Ka jefa sandarka (saiya jefa ta) a yayin dayagan ta tana motsi,kai kace wata micijiyace karama, saiya girka aguje bai waiwayo ba, (Ubangiji yace,) Ya Musa kada kaji tsoron ta, haƙiƙa ni jakadu basa jin tsoro a guna (game da micijiyako wanin ta)
11. Sai dai wanda ya zalinci kansa, sannan ya musanya kyakkyawa bayan mummuna, to haƙiƙa Ni mai gafara ne mai jinkai (a gareshi, zan karɓi tubansa in yafe masa).
12. Ka shigar da hannun ka cikin wuyar rigar ka ta fito fara fat bada muni ba, na albaras, tana da haske wanda yake dumdume idanu a cikin ayoyi guda tara abin aikowa da ita izuwa Fir'auna da mutanensa, haƙiƙa su sun kasance mutane fasikai.
13. Yayin da ayoyinmu sukazo musu halin kasancewar su masu haske mabayyana Sukace, "Wannan tsafi ne mabayyani".

وَجَحَدُواْ بِهَا وَاسْتَيْقَنَتْهَا أَنفُسُهُمْ ظُلْماً وَعُلُوّاً فَانظُرْ كَيْفَ
كَانَ عَاقِبَةُ الْمُفْسِدِينَ ﴿14﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا دَاوُودَ وَسُلَيْمَٰنَ عِلْماً
وَقَالَا الْحَمْدُ لِلَّهِ الَّذِے فَضَّلَنَا عَلَىٰ كَثِيرٍ مِّنْ عِبَادِهِ الْمُؤْمِنِينَ ﴿15﴾
وَوَرِثَ سُلَيْمَٰنُ دَاوُودَ وَقَالَ يَٰٓأَيُّهَا النَّاسُ عُلِّمْنَا مَنطِقَ الطَّيْرِ
وَأُوتِينَا مِن كُلِّ شَےْءٍ إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ الْفَضْلُ الْمُبِينُ ﴿16﴾
وَحُشِرَ لِسُلَيْمَٰنَ جُنُودُهُ مِنَ الْجِنِّ وَالْإِنسِ وَالطَّيْرِ
فَهُمْ يُوزَعُونَ ﴿17﴾ * حَتَّىٰٓ إِذَآ أَتَوْاْ عَلَىٰ وَادِ النَّمْلِ قَالَتْ نَمْلَةٌ
يَٰٓأَيُّهَا النَّمْلُ ادْخُلُواْ مَسَٰكِنَكُمْ لَا يَحْطِمَنَّكُمْ سُلَيْمَٰنُ
وَجُنُودُهُ وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿18﴾ فَتَبَسَّمَ ضَاحِكاً مِّن قَوْلِهَا
وَقَالَ رَبِّ أَوْزِعْنِے أَنْ أَشْكُرَ نِعْمَتَكَ الَّتِے أَنْعَمْتَ عَلَيَّ
وَعَلَىٰ وَالِدَيَّ وَأَنْ أَعْمَلَ صَالِحاً تَرْضَاهُ وَأَدْخِلْنِے بِرَحْمَتِكَ
فِے عِبَادِكَ الصَّالِحِينَ ﴿19﴾ وَتَفَقَّدَ الطَّيْرَ فَقَالَ مَا لِيَ لَا أَرَى
الْهُدْهُدَ أَمْ كَانَ مِنَ الْغَآئِبِينَ ﴿20﴾ لَأُعَذِّبَنَّهُ عَذَاباً شَدِيداً
أَوْ لَأَاذْبَحَنَّهُ أَوْ لَيَأْتِيَنِّے بِسُلْطَٰنٍ مُّبِينٍ ﴿21﴾ فَمَكَثَ غَيْرَ بَعِيدٍ
فَقَالَ أَحَطتُّ بِمَا لَمْ تُحِطْ بِهِ وَجِئْتُكَ مِن سَبَإٍ بِنَبَإٍ يَقِينٍ ﴿22﴾

ثمن

14. Sukayi musun ta a haƙiƙa kuwa kansu sun tabbata wannan daga Allah take don zalinci da girman kai (ga barin imani da abinda Annabi Musa yazo dashi). Ka dubaka gani (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama) yaya karshen mabarnata ya kasance.

(ƘISSAR ANNABI DAWUDA ALAIHISSALAMU DAGA NI,IMOMIN ALLAH TA'ALA A BISA ANNABI DAWURIU DASULAIMANU DA KIS.SAR TURURUWA)

15. Haƙiƙa Mun baiwa Annabi Dawuriu dasulaimanu ilimi (na alkalanci) tsakanin mutane da furucin tsuntsu da wanin wannan, sukace suna masu godiyaga Allah, yabo ya tabbata ga Allah wanda yafifitamu (da Annabci da hore aljannu da mutane da shaidanu, yafifita mu) bisa yawaicin muminai.

16. Annabi Sulaimanu yagaji Annabi Dawuriu (yagaji annabci da ilimi ba tare da sauran 'yan'uwan basu goma sha tara. Yace Yaku waɗannan mutane, an sanar da mu furucin tsuntsaye, hakana tsiri, da hatsi suna zance dashi yana fahimtar zancensu, an bamu daga kowane abu da ake baiwa Annabawa da sarakuna, haƙiƙa wannan abin bayarwan nari lalle shine falala mabayyani.

17. An tara rundunar Sulaimanu gareshi na aljanu da mutane da tsuntsaye (a cikin wata tafiya tasa) to su ana tattara su sannan a kora su.

18. Har sukazo bisa zazan tururuwa (a Da'ifa yake)[1] sai tumruwa Tace wato sarauniyar tumruwa i "Yaku waɗannan tumruwa i, ku shiga ramukan ku (wato dakunan ku,) kadasulaimanu da rundunarsa su karYaku, alhali su badasun sani ba!" (An saukar da tururuwa masaukar masu hankali a cikin zance sabodata samu damar zance dasu).

19. To sai Annabi Sulaimanu yayi murmushi yana mai dariya saboda maganar ta (alhali yaji muryar ta daga mil uku, Ance isk a ce ta kai masa wannan zance) saiya tsare rundunar tasa lokacin dayayi tsinka ye a bisa zazan nasu har suka shiga dakunan su, rundunar tasa kuwa kashi biyu ne, mahaya dayan sad, wato masu tafiya kan sawun su a cikin wannan tafiya) yace "Ubangijina, kimsa min in godewa ni'imarka, wacce ka ni'imta gare ni da itada kuma mahaifana kuma in yi aiki nagari wanda zaka yarda dashi ka shigar dani saboda jinƙan ka cikin bayi managarta annabawa da waliyyai".

(ILIMIN KIMIYYA)

20. Ya binciki tsuntsu alhuduhudu (wanda yake ganin ruwa ƙarƙashin ƙasa, yake shiryarwa a kansa da tsatstsagarsa a cikin ta, sai shaidanu su fito dashi saboda bukatar Annabi Sulaimanu saboda sallah, shine su feɗe fuskar ƙasa ruwa ya bayyana kamar yadda ake feɗe akuya, to sai bai ga alhuduhudun ba). Sai yace, "Saboda Menene ni ban ga alhuduhudu ba, (shin wani abu ne ya afku gare ni yan hana ni ganin sa,) ko ko ya kasance cikin fakakku, bangan shiba saboda fakuwar sa? Yayin daya tabbatar da fakuwar sa).

21. Sai yace, "lalle zan yi masa azaba mai tsanani (da cisge gyawaskar sa wato gashin sa da jelar sa da jefa shi a cikin rana bazai iya hanuwa daga kwari masu cizo ba!) ko lalle in yanka shi (dayanke makogwaron sa) ko yazo min da hujja mabayyaniya (a kan hanzarin dayayi".)

22. To saiya zauna ba a nesa ba (daga zamanin, yazo yana mai tawali'u ga Annabi Sulaimanu da daga kansa, da sakin jelarsa da fikafikansa, sai yayi masa rangwame, ya tambaye shi da abinda yagamu dashi a halin baya nan,) sai yace na kewaye abinda baka kewaye da sanin sa ba, nazo maka daga Sabada labari na (yakini) (wato na dahir).

1). wadin - namli yana nan a da'ifa har izuway yau haka ake kiransa – sanajiy

إِنِّي وَجَدتُّ ٱمْرَأَةً تَمْلِكُهُمْ وَأُوتِيَتْ مِن كُلِّ شَيْءٍ وَلَهَا عَرْشٌ
عَظِيمٌ ﴿23﴾ وَجَدتُّهَا وَقَوْمَهَا يَسْجُدُونَ لِلشَّمْسِ مِن دُونِ ٱللَّهِ
وَزَيَّنَ لَهُمُ ٱلشَّيْطَٰنُ أَعْمَٰلَهُمْ فَصَدَّهُمْ عَنِ ٱلسَّبِيلِ فَهُمْ
لَا يَهْتَدُونَ ﴿24﴾ أَلَّا يَسْجُدُوا لِلَّهِ ٱلَّذِي يُخْرِجُ ٱلْخَبْءَ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ وَيَعْلَمُ مَا تُخْفُونَ وَمَا تُعْلِنُونَ ﴿25﴾ ٱللَّهُ لَا إِلَٰهَ
إِلَّا هُوَ رَبُّ ٱلْعَرْشِ ٱلْعَظِيمِ ۩ ﴿26﴾ ۞ قَالَ سَنَنظُرُ أَصَدَقْتَ
أَمْ كُنتَ مِنَ ٱلْكَٰذِبِينَ ﴿27﴾ ٱذْهَب بِّكِتَٰبِي هَٰذَا فَأَلْقِهْ إِلَيْهِمْ ثُمَّ تَوَلَّ
عَنْهُمْ فَٱنظُرْ مَاذَا يَرْجِعُونَ ﴿28﴾ قَالَتْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلْمَلَؤُا إِنِّيٓ أُلْقِيَ إِلَيَّ
كِتَٰبٌ كَرِيمٌ ﴿29﴾ إِنَّهُ مِن سُلَيْمَٰنَ وَإِنَّهُ بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ﴿30﴾
أَلَّا تَعْلُوا عَلَيَّ وَأْتُونِي مُسْلِمِينَ ﴿31﴾ قَالَتْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلْمَلَؤُا أَفْتُونِي
فِي أَمْرِي مَا كُنتُ قَاطِعَةً أَمْرًا حَتَّىٰ تَشْهَدُونِ ﴿32﴾ قَالُوا نَحْنُ
أُولُوا قُوَّةٍ وَأُولُوا بَأْسٍ شَدِيدٍ ﴿33﴾ وَٱلْأَمْرُ إِلَيْكِ فَٱنظُرِي مَاذَا
تَأْمُرِينَ ﴿34﴾ قَالَتْ إِنَّ ٱلْمُلُوكَ إِذَا دَخَلُوا قَرْيَةً أَفْسَدُوهَا
وَجَعَلُوا أَعِزَّةَ أَهْلِهَا أَذِلَّةً وَكَذَٰلِكَ يَفْعَلُونَ ﴿35﴾
وَإِنِّي مُرْسِلَةٌ إِلَيْهِم بِهَدِيَّةٍ فَنَاظِرَةٌ بِمَ يَرْجِعُ ٱلْمُرْسَلُونَ ﴿36﴾



23. "Ni na samu wata mace tana mallakar su (ita sarauniyace a garinsu sunan ta Bilkisu) an bata daga kowane abu (da sarakuna suke bukata dashi na daga kayan fada da tanaji,) gado mai girma ya tabbata gare ta, (tsawon sa zira'i tamanin, fadin sa zira'i arba'in, cirawar sa sama zira'i talatin, abin kerawa da zinare da azurfa wato a maimakon katako abindajewa da lu'ulu'i dayakutu da kore zabarjadu da zumurmzu wato kafafuwan sa na jan yakutu da koren zabarjadu, yana da dakuna guda bakwai kowanne daki ƙofa abar kullewa bissa kowane akwai ƙyaure a kulle).
24. "Na same tada mutanen ta suna sujada ga rana da wata ba Allah ba, shidan ya kawata musu aikin su ya hana su ga barin hanyar tsira, su basu bin shiriya
25. "Bazasu shiriyaba cewa suyi sujada ga Allah ba, wanda yake fitar da abinda ke ɓoye a cikin sammai da kassai kuma yake sane da abinda suke boyewa da wanda suke bayyanawa.
26. Babban Sarki Allah, ba abin bautawa da gaskiya sai shi, Ubangijin Al'arshi mai girma, (wanda yafi gadon Bilkisa).
27. Annabi Sulaimanu alaihissalamu ya faɗa ga alhuduhudu "Da sannu zamu dubamu gani ka gaskata a cikin labarin daka bamu ko ka kasance daga cikin makaryata". Sannan ya shiryar dasu a kan ruwa aka fito dashi suka sha suka ƙoshi sukayi alwala sukayi sallah, sannan Annabi sulaimanu ya rubuta musu takarda, surar takardar: Daga bawan Allah Sulaimanu dan Dawuriu izuwa Bilkisa Sarauniyar Saba.Gaisuwa ga wanda yabi shiriya, bayan haka, kar kuyi girman kai gare ni, kuzo min kuna masu mika wuya, sannan ya yimke takardar da miski, ya sa tambarinsa a kai, sannan yace da huduhudu:)
28. "Tafi da takardata wannan ka jefa ta izuwa garesu (Bilkisa da mutanen ta) sannan ka juyaga barin su (ko ka tsaya daf dasu) ka duba me zasu komo ma (dashi na daga jawabi, saiya karbe ta ya je mata, akwai rundunar ta sun kewaye ta ya jefa ta a kan cinyar ta yayin data gan shi saita rinka makyarkyata, saita ji tsoro mai yawa, sannan ta karanta abinda yake ciki ta fahince shi").
29. Sannan Tace da manyan mutanen ta "Yaku waɗannan mutanena ni an jeho mun littafi mai girma.
30. "Shin ne haƙiƙa lamarin daga Sulaimanu kuma haƙiƙa abindata kunsa: BISMILLAHIR-RAHMANIR-RAHIM
31. "Cewa kada kuyi shisshigi a kaina, kuzo min kuna masu mikawuya".
32. Tace, "Yaku wannan jama'a, kuyi min fatawa cikin al'amarina, (wato kuyi min nuni,) Ni bazan yanke da wani al'amari ba sai kun halarce ni".
33. Sukace, "Mu ma'abota karfi ne ma'abota zafi ne (a cikin yaki).
34. "Laman na gare ki, ki duba me za ki umarce mu dashi (mu biki)".
35. Tace, "Haƙiƙa sarakuna in suka shiga alƙarya saisu rnsa ta, su mayar da manya manyan mutanen ta wulakantattu, hakana zasu aikata mana, (su masu aiko da wannan takarda).
36. " Haƙiƙa ni zan aike musu da kyauta na ga abinda jakadu zasu komo min (dashi na karɓar kyautar nan ko maido ta, in sarki ne zai karɓe ta, in Annabi ne bazai karɓa ba". Ta aika masa da bayi maza da mata dubu daidai wa daida, wato mata dari biyar maza dari biyar da tubali na zinare dari biyar da kambi abindajewa da jauharori, da almiski da al'ambar da wanin wancananka tareda manzoda takarda, sai alhuduhudu yayi gaggawa izuwa Annabi Sulaimanu ya tsegunta masa wannan labari, sai yayi umarni a gina = tubala na zinare da azurfa tamfar yadda ake yin na yumbu a sanya ta kamar dabe tun daga gurinsa har izuwa farsahi tara, wato yana fage suna gina garu mai tsaho daura dashi na zinare da azurfa, kuma su zoda mafi kyan dabbobina sarari dana kagi, su zo dasu da 'ya'yan aljanu dama da hauni).

فَلَمَّا جَآءَ سُلَيْمَٰنَ قَالَ أَتُمِدُّونَنِ بِمَالٍ فَمَآ ءَاتَىٰنِۦَ ٱللَّهُ خَيْرٌ مِّمَّآ ءَاتَىٰكُم
بَلْ أَنتُم بِهَدِيَّتِكُمْ تَفْرَحُونَ ﴿٣٦﴾ ٱرْجِعْ إِلَيْهِمْ فَلَنَأْتِيَنَّهُم بِجُنُودٍ لَّا قِبَلَ
لَهُم بِهَا وَلَنُخْرِجَنَّهُم مِّنْهَآ أَذِلَّةً وَهُمْ صَٰغِرُونَ ﴿٣٧﴾ قَالَ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلْمَلَؤُاْ أَيُّكُمْ يَأْتِينِى بِعَرْشِهَا قَبْلَ أَن يَأْتُونِى مُسْلِمِينَ ﴿٣٨﴾ قَالَ عِفْرِيتٌ
مِّنَ ٱلْجِنِّ أَنَا۠ ءَاتِيكَ بِهِۦ قَبْلَ أَن تَقُومَ مِن مَّقَامِكَ وَإِنِّى عَلَيْهِ لَقَوِىٌّ
أَمِينٌ ﴿٣٩﴾ قَالَ ٱلَّذِى عِندَهُۥ عِلْمٌ مِّنَ ٱلْكِتَٰبِ أَنَا۠ ءَاتِيكَ بِهِۦ قَبْلَ
أَن يَرْتَدَّ إِلَيْكَ طَرْفُكَ فَلَمَّا رَءَاهُ مُسْتَقِرًّا عِندَهُۥ قَالَ هَٰذَا مِن فَضْلِ رَبِّى
لِيَبْلُوَنِىٓ ءَأَشْكُرُ أَمْ أَكْفُرُ وَمَن شَكَرَ فَإِنَّمَا يَشْكُرُ لِنَفْسِهِۦ
وَمَن كَفَرَ فَإِنَّ رَبِّى غَنِىٌّ كَرِيمٌ ﴿٤٠﴾ ۞ قَالَ نَكِّرُواْ لَهَا عَرْشَهَا نَنظُرْ أَتَهْتَدِىٓ
أَمْ تَكُونُ مِنَ ٱلَّذِينَ لَا يَهْتَدُونَ ﴿٤١﴾ فَلَمَّا جَآءَتْ قِيلَ أَهَٰكَذَا عَرْشُكِ
قَالَتْ كَأَنَّهُۥ هُوَ وَأُوتِينَا ٱلْعِلْمَ مِن قَبْلِهَا وَكُنَّا مُسْلِمِينَ ﴿٤٢﴾
وَصَدَّهَا مَا كَانَت تَّعْبُدُ مِن دُونِ ٱللَّهِ إِنَّهَا كَانَتْ مِن
قَوْمٍ كَٰفِرِينَ ﴿٤٣﴾ قِيلَ لَهَا ٱدْخُلِى ٱلصَّرْحَ فَلَمَّا رَأَتْهُ حَسِبَتْهُ لُجَّةً
وَكَشَفَتْ عَن سَاقَيْهَا قَالَ إِنَّهُۥ صَرْحٌ مُّمَرَّدٌ مِّن قَوَارِيرَ ﴿٤٤﴾ قَالَتْ
رَبِّ إِنِّى ظَلَمْتُ نَفْسِى وَأَسْلَمْتُ مَعَ سُلَيْمَٰنَ لِلَّهِ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٤٥﴾

ثمن

37. To yayin da jakada ya zowa Annabi Sulaimanu, mabiyansa suna tare dashi da hadiya, sai yace, "Shin kwa kare ni da dukiya? Abinda Allah ya bani (na annabci da mulki) shine mafifici (daga abinda ya baku na duniya,) Kai bari, ku dai kuna farin ciki ne da kyautar ku (saboda alfahari da tarkace-tarkacen du duniya).
38. Koma izuwa garesu (da abinda ka zo dashi na hadiya,) lalle zamu zo musu da runduna wadda basu da iko dasu kuma lalle zamu fishshe su daga garinsu (birnin Saba, an ambace ta dasunan uban kabilarsu,) zamu fishshe su suna. wulakantattu alhali su kaskastantu ne su, (in basu zo mun suna masu mika wuya ba. Zamanin da manzo yakoma musu da wannan kyauta saita sanya ɗaki gadonta cikin bakwai daga cikin katangar gidan ta, gidan nata kuma yana cikin gida bakwai ta kulle kofofin ta sanya masu tsaro a kanta ta shiri tahowa izuwa Annabi Sulaimanu donta ga abindazai umarce ta dashi, saita maraito a cikin makwayo dubu goma sha biyu (12,000) kowane makwayo[1] dubbai tana tare dashi har izuwa kusa da Annabi Sulaimanu da mil uku, to sai yayi hasashe da ita).
(KARAMOMIN WALIYYAI NA ALJANU DA MUTANE DA FIFITA WALIYYIN MUTUM DANA ALJAN)
39. Yace, "Yaku manyan waɗannan jama'a, wanenen ku zaizo min da gadonta tun kafin su zo min suna masu mika wuya?" (Masu bi kan karbar sa gaban wannan ba bayan sa ba.)
40. Sai wani gwarzo daga aljanu (wato mai tsananin karfi) yace, "Ni zan zo maka dashi tun kafin ka tashi daga mazaunin shari'arka (wato shine daga safiya izuwa rabin wuni) Haƙiƙa ni mai karfi ne amintacce ne ga abinda yake cikinsa na jauharori da wanin ta. Annabi Sulaimanu alaihissalamu yace ina son mafi gaggawa daga wancananka.)
41. Sai wanda ilimi na daga littafi ke gurin sa yace, (wato Asifu ɗan Barhaya wato shine 'Ismillahil-aazam' wanda idan an yi addu'a dashi yake amsawa take yace, "Ni zan zo maka dashi tun kafin idonka yakomo gareka (idan kayi dubadashi izuwa wani abu" sai yace duba izuwa sama, saiya duba ta, sannan yakomar da idanunsa, saiya sameshi abin ajiyewa nan gaba gareshi a cikin dubansa izuwa sama ne Asifu ya roka Ismullahil-aazamu, ya roki Allah yazo masa dashi, saiya tabbata shine ya gudana ƙarƙashin ƙasa har ya gudana ƙarƙashin gadon Annabi Sulaimanu alaihissalamu) yayin dayagan shi matabbaci gareshi sai yace, "Wannan kawo shi din nan yana daga falalar Ubangijina donya jarrabe ni na gode masa ko na butulce masa, wanda ya gode wa ni'ima, to dahir dai ya gode don kansa (domin sakamakon godiyar nan nasa ne,) wanda ya butulce ni'ima haƙiƙa Ubangijina mawadaci ne gabarin godiyarsa mai karamci ne da baiwa a bisa wanda ya butulce masa".
42. Sai yace, "Ku jirkita gadonta gare a ta (izuwa halin daza tayi musun sa in ta gan shi) mu gani ta shiriya izuwa sanin sa, ko ta kasance daga waɗanda bazasu shiriya (izuwa sanin abinda aka jirkita a garesu ?" Yanufi jarraba hankalin tada wancananka yayin da akace dashi akwai motsuwa cikin hankalin ta, suka jirkita shi da ƙari ko ragi).
43. Yayin datazo sai akace da ita "Shin kamar haka gadonki yake?" Saitace, "Kai kace shi shine", (wato ta sanshi ta kwatance garesu kamar yadda suka shigar da kwatance gare ta, don bai ce da ita shin wannan gadon ki ne ba? Dayace haka da saitace na'am gadona ne. Annabi Sulaimanu alaihissalamu ya faɗi yayin data ci jarrabawa, wato ya tabbata tana da ma'arifa da ilimi) an bamu ilimi tun gaban ta, mun kasance masu mika wuya (ya faɗi wannan ne don ɗaiɗaita godiyar Ubangiji).
44. Abinda take bautawa ba Allah ba, ya tare ta ga bautar Allah Subhanahu wata'ala haƙiƙa ita ta kasance daga mutane kafirai.
45. Ance da ita kishigo wannan rufi rufi ne na gilas fari (wato kaskon karau ruwan dadi mai kwarara yana ƙarƙashinsa, akwai kifi da kwaɗi da dabbobin ruwa Annabi Sulaimanu ya zubasu a cikin ruwa yayin da aka ce dashi makyangyamuntada dugad-uganta kamar na jaki suke. A zamanin data gan shi saita zaci kunzumin ruwa , na) ta yaye ga buran makyangyamanta guda biyu don (ta kutsa a cikin ruwan, Annabi Sulaimanu yana kan gadonsa a gaban rufin sai yaga makyan gyamattada sawayenta kyawawa). Sai yace haƙiƙa shi rufi ne mai santsi (na kasaken karau ya kira ta izuwa Musulunci).

1) MAKWAYO: HAKIMI

وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا إِلَىٰ ثَمُودَ أَخَاهُمْ صَٰلِحًا أَنُ اعْبُدُوا اللَّهَ فَإِذَا هُمْ
فَرِيقَانِ يَخْتَصِمُونَ ﴿47﴾ قَالَ يَٰقَوْمِ لِمَ تَسْتَعْجِلُونَ بِالسَّيِّئَةِ
قَبْلَ الْحَسَنَةِ لَوْلَا تَسْتَغْفِرُونَ اللَّهَ لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ ﴿48﴾ قَالُوا اطَّيَّرْنَا
بِكَ وَبِمَن مَّعَكَ قَالَ طَٰٓئِرُكُمْ عِندَ اللَّهِ بَلْ أَنتُمْ قَوْمٌ تُفْتَنُونَ ﴿49﴾ وَكَانَ
فِي الْمَدِينَةِ تِسْعَةُ رَهْطٍ يُفْسِدُونَ فِي الْأَرْضِ وَلَا يُصْلِحُونَ ﴿50﴾ قَالُوا
تَقَاسَمُوا بِاللَّهِ لَنُبَيِّتَنَّهُۥ وَأَهْلَهُۥ ثُمَّ لَنَقُولَنَّ لِوَلِيِّهِۦ مَا شَهِدْنَا مَهْلِكَ أَهْلِهِۦ
وَإِنَّا لَصَٰدِقُونَ ﴿51﴾ وَمَكَرُوا مَكْرًا وَمَكَرْنَا مَكْرًا وَهُمْ
لَا يَشْعُرُونَ ﴿52﴾ فَانظُرْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ مَكْرِهِمْ إِنَّا دَمَّرْنَٰهُمْ
وَقَوْمَهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿53﴾ فَتِلْكَ بُيُوتُهُمْ خَاوِيَةًۢ بِمَا ظَلَمُوا إِنَّ فِي ذَٰلِكَ
لَأٓيَةً لِّقَوْمٍ يَعْلَمُونَ ﴿54﴾ وَأَنجَيْنَا الَّذِينَ ءَامَنُوا وَكَانُوا يَتَّقُونَ ﴿55﴾
وَلُوطًا إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِۦ أَتَأْتُونَ الْفَٰحِشَةَ وَأَنتُمْ تُبْصِرُونَ ﴿56﴾
أَئِنَّكُمْ لَتَأْتُونَ الرِّجَالَ شَهْوَةً مِّن دُونِ النِّسَآءِ بَلْ أَنتُمْ قَوْمٌ تَجْهَلُونَ ﴿57﴾
فَمَا كَانَ جَوَابَ قَوْمِهِۦ إِلَّا أَن قَالُوا أَخْرِجُوا ءَالَ لُوطٍ
مِّن قَرْيَتِكُمْ إِنَّهُمْ أُنَاسٌ يَتَطَهَّرُونَ ﴿58﴾ فَأَنجَيْنَٰهُ وَأَهْلَهُۥ إِلَّا امْرَأَتَهُۥ
قَدَّرْنَٰهَا مِنَ الْغَٰبِرِينَ ﴿59﴾ وَأَمْطَرْنَا عَلَيْهِم مَّطَرًا فَسَآءَ مَطَرُ الْمُنذَرِينَ ﴿60﴾

46. Tace, "Ubangijina, haƙiƙa ni na zalinci kaina (da bautar waninka) na mika wuya tareda Annabi Sulaimanu don Allah Ubangijin talikai (yanufi auren ta saiyaki saboda gashin makyangyamarta, sai shaidanu sukayi masa nura saiya kawar da gashin nan da ita nurar, wato farar ƙasar Turawa, saiya kawar da gashin da ita wannan farar ƙasar saiya aure ta yaso ta ya tabbatar da ita a kan mulkin ta, ya kasance yana ziyarar ta sau dayakowane wata, yana zama nan gare ta kwana uku, mulkin ta ya kare da karewar mulkin Annabi Sulaimanu alaihissalamu, an ruwaito cewa shi an sarauta shi yana dan shekara goma sha uku, ya mutu yana dan shekara hamsin da uku. Tsarki ya tabbatar wa wanda bakarewa ga dauwamar mulkinsa.)

(ƘISSAR ANNABI SALIHU DA MUTANENSA SAMUDAWA)

47. Haƙiƙa mun aiko Annabi Salihu izuwa samudawa dan uwansu na kabila, cewa ku kadaita Allah, sai gasu jama'a guda biyu suna husuma (a cikin addini, jama'ar mummunai tun zamanin da aka aiko shi izuwa garesu da jama'ar kafirai).

48. Yace (da masu ƙaryatawa) "Yaku mutanena, donme kuke garaje da mummunan aiki gaban kyakykyawa? (wato azaba gaban rahama lokacin da kukace in abinda ka zo mana dashi gaskiya ne to kazo mana da azaba.) To donme baku nemi gafarar Allah ba (daga shirka ko ajikan ku?) sukace.

49. Munyi shu'umi ne dakai da wađanda suke tare dakai (na daga muminai lokacin da akayi musu fari kuma sukayi yunwa,) yace "Shu'umin ku yana wurin Allah, (Allah ne yazo muku dashi). Bari, kudai mutane ne da ake jarrabar ku (da hairi da sharri").

50. A cikin birnin Samuda akwai mutum tara suna barna a cikin ƙasa (da sabanni, yana daga sabannin suna ranta dinarai da dirhamai,) su basa yin gyara da biyayyar Allah.

51. Sukace, "sashinsu yace da sashi ku rantse da Allah, lalle zamu kwanke masa shi da mutanensa, ai zamu kashe su da daddare, sannan zamu fada ga waliyyinsa (watau mai jan jininsa)" bamu halicci gurin halakar mutanensu ba, haƙiƙa lalle mu magasgata ne".

52. Sunyi ƙulle -ƙulle, mu kuma munyi musu sakamakon ƙulle ƙullen nasu da gaggauta musu ukuba alhali su basu sani ba.

53. To ka dubaka gani ƙaƙa ƙarshen ƙulle-ƙullen nasu ya kasance cewa mu mun halakar da mutanensu baki daya (da tsawar Mala'ika Jibrilu ko da jefawar duwatsu da maramarai dasuke ganin ta, basa ganin su!) (malaikun)

54. Wancananka gidaddajinsune mawofinta saboda kafircinsu, akwai aya cikin waneananka ga mutane da sukasan (hukuncinmu).

55. Muka tserar da wađanda suka bada gaskiya (Annabi Salihu da mutanensa dubu hudu) sun kasance masu tsoron shirka ne.

(ƘISSAR ANNABI LUĐU ALAIHISSALAMU DA MUTANENSA)

56. Ambaci Annabi Luđu zamanin daya fada ga mutanensa, "Donme kuke aikata aikin barna (neman maza) alhali kuna kallon junan ku (don kutsawa a cikin sabon Allah).

57. Shin kwa dinga zuwa wa mazaje don sha'awa ba mata ba, bari ku mutane ne da kuka jahilci karshen al'amarinku.

58. Jawabin mutanensa bai kasance ba sai fađin su, "Ku fitar da mutanen Annabi Luđu daga alƙaryarku, haƙiƙa su mutane ne dasuke tsarkaka (ga barin duburar maza").

59. To sai muka tserar dashi da iyalinsa sai mata tasa, mun sanya ta daga cikin masu wanzuwa (cikin azaba).

60. Muka kunzo ruwa a kansu (shi ruwan nan duwarwatsune na sijilu ta halakar dasu,) to tur, ruwan ababan wa gargadi (da azaba, wannan ruwanasu.)

حزب

۞ قُلِ الْحَمْدُ لِلَّهِ وَسَلَامٌ عَلَىٰ عِبَادِهِ الَّذِينَ اصْطَفَىٰ
ءَآللَّهُ خَيْرٌ أَمَّا تُشْرِكُونَ ﴿59﴾ أَمَّنْ خَلَقَ السَّمَاوَاتِ
وَالْأَرْضَ وَأَنزَلَ لَكُم مِّنَ السَّمَاءِ مَاءً فَأَنبَتْنَا بِهِ
حَدَائِقَ ذَاتَ بَهْجَةٍ مَّا كَانَ لَكُمْ أَن تُنبِتُوا شَجَرَهَا
أَإِلَٰهٌ مَّعَ اللَّهِ بَلْ هُمْ قَوْمٌ يَعْدِلُونَ ﴿60﴾ أَمَّن جَعَلَ
الْأَرْضَ قَرَارًا وَجَعَلَ خِلَالَهَا أَنْهَارًا وَجَعَلَ لَهَا رَوَاسِيَ وَجَعَلَ
بَيْنَ الْبَحْرَيْنِ حَاجِزًا أَإِلَٰهٌ مَّعَ اللَّهِ بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿61﴾
أَمَّن يُجِيبُ الْمُضْطَرَّ إِذَا دَعَاهُ وَيَكْشِفُ السُّوءَ وَيَجْعَلُكُمْ
خُلَفَاءَ الْأَرْضِ أَإِلَٰهٌ مَّعَ اللَّهِ قَلِيلًا مَّا تَذَكَّرُونَ ﴿62﴾
أَمَّن يَهْدِيكُمْ فِي ظُلُمَاتِ الْبَرِّ وَالْبَحْرِ
وَمَن يُرْسِلُ الرِّيَاحَ نُشْرًا بَيْنَ يَدَيْ رَحْمَتِهِ
أَإِلَٰهٌ مَّعَ اللَّهِ تَعَالَى اللَّهُ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿63﴾
أَمَّن يَبْدَؤُا الْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُ وَمَن يَرْزُقُكُم مِّنَ السَّمَاءِ وَالْأَرْضِ
أَإِلَٰهٌ مَّعَ اللَّهِ قُلْ هَاتُوا بُرْهَانَكُمْ إِن كُنتُمْ صَادِقِينَ ﴿64﴾ قُل لَّا يَعْلَمُ مَن
فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ الْغَيْبَ إِلَّا اللَّهُ وَمَا يَشْعُرُونَ أَيَّانَ يُبْعَثُونَ ﴿65﴾

(DALILAI MASU KADAITARWA DA IKONSA)

61. Ka faɗa (Ya Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama) Godiya ta tabbata ga Allah (a bisa halakar kafiran al'umar suka da wuce) gaisuwa ta tabbata bisa bayinsa wanda ya zabe su (sune Annabawa da Sahabbai da muminai har izuwa tashin kiyama.) Shin Allah shine yafi amfani (ga wanda yake bauta masa) ko abinda kuke shirkantawa[1] (iyayen giji su sukafi ga masu bauta mata?)

62. Bari! Shin wanda ya halicci sammai da ƙassaiya saukar da ruwa daga sama a gare ku, muka tsirar da gonaki dashi ma'abota kyau, bazai yuwu gareku ku tsirar da itaciyarta ba saboda rashin ikon ku a kansa. Shin akwai wani Ubangiji tare da Allah (dazai taimake shi a kan wancananka? Babu.) Bari! Sudai mutane ne dasuke shirkantawa (wanin Allah tareda Allah).

63. Shin wanda ya shimfida ƙasa matabbaci (bata juyewa da mutanen ta) yasanya ƙoramu a tsastsakinta yasanya duwatsu gare ta (daya kafa ƙasa da ita) yasanya shamaki tsakanin kogi biyu (kogin zaki dana zartsi, dayansu baya cudanya da daya,) Shin akwai abin bautawa tareda Allah? ƙadan ne kawai kuke wa'azantuwa, bari yawancin su basu san kaɗaita Allah ba.

64. Bari! Shin wanda yake amsawa mai tsananin bukata idan ya roke shi yake yaye matsuwa ga waninsa ga barinsa, yake sanya ku masu maye ƙasa (wato kowane tsara yake maye tsaran da ke gabansa wato kami) Shin akwai abin bautawa tareda Allah? Kadan ne kwarai kuke wa'azantuwa.

65. Bari! Shin wanda yake shiriyar ku (ya zuwa manufarku) a cikin duffan sarari da kogi, yake shiriyar kuda taurari da daddare, yake shiriyar kuda alamomin ƙasa da rana, da wanda yake sakko iskoki abin ɗaiɗaitawa nan ga bannin rahamarsa (wato ruwa,) Shin akwai abin bautawa tareda Allah? Allah ya girmama ga abinda suke shirkanta waninsa dashi.

66. Shin wanda yake farar halitta (cikin mahaifa daga digon maniyyi a cikin mahaifa,) sannan ya mayar dashi (bayan mutuwa, ko da bakuyi furuci da mayar dashi ba) wanene mai azurta kuda ruwa daga sama da kasa? (Da tsiri). Shin akwai wani abin bautawa tareda Allah? (Ai ba mai aikata wani abu daga abinda aka ambata sai Allah. Ka fadaya Muhammadu, ku zoda hujjar ku in kun kasance magasgata (cewa idan akwai abin bautawa taredani daya aikata abinda aka ambata din nan. Suka tambaye shi lokacin tashin ƙiyama sai Allah ya saukar da);

67. Cene, "Wanda yake cikin sammai ko ƙassai basu san gaibu ba, ba wanda yasan gaibu (na Mala'ikuda mutane). Sai Allah kawai, kafiran Makka basu san wane lokaci za a tashe su ba (hakana ma waɗansunsu).

1) Manzon Allah (S.A.W) ya kasance inya karanta wannan ayaya kance "ALLAHU KHAIRUN - WA - ABKA - WA - AJALLU - WA -AKRAMU". - Sanajiy -.

ثمن

بَلِ ٱدَّٰرَكَ عِلْمُهُمْ فِي ٱلْآخِرَةِۚ بَلْ هُمْ فِي شَكٍّ مِّنْهَاۖ
بَلْ هُم مِّنْهَا عَمُونَ ﴿٦٦﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَءِذَا كُنَّا
تُرَٰبًا وَءَابَآؤُنَآ أَئِنَّا لَمُخْرَجُونَ ﴿٦٧﴾ لَقَدْ وُعِدْنَا هَٰذَا
نَحْنُ وَءَابَآؤُنَا مِن قَبْلُ إِنْ هَٰذَآ إِلَّآ أَسَٰطِيرُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٦٨﴾
قُلْ سِيرُواْ فِي ٱلْأَرْضِ فَٱنظُرُواْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ
ٱلْمُجْرِمِينَ ﴿٦٩﴾ وَلَا تَحْزَنْ عَلَيْهِمْ وَلَا تَكُن فِي ضَيْقٍ
مِّمَّا يَمْكُرُونَ ﴿٧٠﴾ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلْوَعْدُ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٧١﴾
قُلْ عَسَىٰٓ أَن يَكُونَ رَدِفَ لَكُم بَعْضُ ٱلَّذِي تَسْتَعْجِلُونَ ﴿٧٢﴾
وَإِنَّ رَبَّكَ لَذُو فَضْلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَشْكُرُونَ ﴿٧٣﴾
وَإِنَّ رَبَّكَ لَيَعْلَمُ مَا تُكِنُّ صُدُورُهُمْ وَمَا يُعْلِنُونَ ﴿٧٤﴾
وَمَا مِنْ غَآئِبَةٍ فِي ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ إِلَّا فِي كِتَٰبٍ مُّبِينٍ ﴿٧٥﴾
إِنَّ هَٰذَا ٱلْقُرْءَانَ يَقُصُّ عَلَىٰ بَنِيٓ إِسْرَٰٓءِيلَ أَكْثَرَ ٱلَّذِي هُمْ
فِيهِ يَخْتَلِفُونَ ﴿٧٦﴾ وَإِنَّهُۥ لَهُدًى وَرَحْمَةٌ لِّلْمُؤْمِنِينَ ﴿٧٧﴾
إِنَّ رَبَّكَ يَقْضِي بَيْنَهُم بِحُكْمِهِۦۚ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٧٨﴾
فَتَوَكَّلْ عَلَى ٱللَّهِۖ إِنَّكَ عَلَى ٱلْحَقِّ ٱلْمُبِينِ ﴿٧٩﴾

(ILIMI NA TASHIN ƘIYAMA)

68. Shin ilimin su ya riskune a cikin Lahira har suka tambayaga lokacin da zata zo? A'a, bari Sudai suna cikin kokwanto gare ta. Bari Sudai makafi ne a gare ta.
69. Waɗanda suka kafirta ga barin tashin ƙiyama Sukace, Shin idan mun kasance turbaya da iyayen mu za a fitar da mu daga ƙaburbura?
70. Haƙiƙa an yi mana alƙawarin wannan mu da iyayenmu tunda, wannan bai kasance ba sai ƙaryace ƙaryacen mutanen farko.
71. Cene, "Kuyi tafiya a cikin ƙasa ku duba yaya karshen masu laifi ya kasance? (Shine halakar dasu da azaba).
72. Kada kayi bakin ciki a kansu,kadaka kasance mai kunci daga abinda suke ma makirci rar rashine ga manzon Allah (s.a.w) (a ciki saboda haƙiƙa mu masu taimako ne a gareka a kansu.)
73. Suna cewa, "Yaushe wannan alƙawari na azaba in kun kasance magasgata (cikinsa.)
74. Cene Yakusan ta ba alin abinda kuke neman garajensa ya kasance ya gwamutsa gare ku. azabar kuma za tazo musu bayan mutuwa.)
75. Haƙiƙa Ubangijinka mai falala ne ga mutane sai dai yawaicin su basa godewa.
76. Haƙiƙa Ubangijinka yasan abinda ƙirajensu take ɓoyewa da abinda suke bayyanawa (da harasan su).
77. Babu wata mai buya a cikin sama ko ƙasa face tana cikin littafi mabayyani, (shine Lauhil-Mahafuzu, yana daga ɓoyayyen iliminsa a zabta kafirai kuma yana cikin iliminsa.)

(ALƘUR'ANI MAI GIRMA DA ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

78. Haƙiƙa wannan Alƙur'ani yana labartawa ga Banu-Isra'ila mafi yawan abinda suke saɓani (cikinsa yake bayani ga abinda aka dauke na sabanin su. Dasun yi riko dashi dasun Musulunta.)
79. Haƙiƙa shi Alƙur'ani shinya ne (daga bata) rahama ne ga muminai.
80. Haƙiƙa Ubangijinka yana hukunci tsakanin su a (tamfar waninsu ranar alƙiyama da hakuncinsa ai da adalcinsa) shine mabuwayi, shine mai sani (da abinda yake hukunci dashi, bazai yar dar wa dayaya saba wa Alƙur'an ba, tamfar da kufirai suka sabawa Annaba wansu a duniya).
81. Ka dogara bisa Allah, (ka amince dashi) kai kana bisa kan gaskiya mabayyaniya, (akiba kyakykyawa takace za kayi nasara a kan kafirai. Sannan yasanya musu makance-makance da kummta, yace;)
82. Haƙiƙa kai baka jiyar da matattu kira, baka jiyar da kurame, baka jiyar dasu kira idan sun girka aguje suna bada baya.
83. Bakaine mai shiryar da makafi ga barin batansu ba, kai baka jiyarwa jin karɓa sai wanda ya bada gaskiya da ayoyinmu (na Alƙur'ani,) to, su suna tsarkakewa (da ayoyinmu na Alƙur'ani wato masu ikhlasi).

إِنَّكَ لَا تُسْمِعُ الْمَوْتَىٰ وَلَا تُسْمِعُ الصُّمَّ الدُّعَاءَ إِذَا وَلَّوْا
مُدْبِرِينَ ﴿82﴾ وَمَا أَنتَ بِهَادِ الْعُمْيِ عَن ضَلَالَتِهِمْ
إِن تُسْمِعُ إِلَّا مَن يُؤْمِنُ بِءَايَاتِنَا فَهُم مُّسْلِمُونَ ﴿83﴾
* وَإِذَا وَقَعَ الْقَوْلُ عَلَيْهِمْ أَخْرَجْنَا لَهُمْ دَابَّةً مِّنَ الْأَرْضِ
تُكَلِّمُهُمْ إِنَّ النَّاسَ كَانُوا بِءَايَاتِنَا لَا يُوقِنُونَ ﴿84﴾
وَيَوْمَ نَحْشُرُ مِن كُلِّ أُمَّةٍ فَوْجًا مِّمَّن يُكَذِّبُ بِءَايَاتِنَا
فَهُمْ يُوزَعُونَ ﴿85﴾ حَتَّىٰ إِذَا جَاءُو قَالَ أَكَذَّبْتُم بِءَايَاتِي
وَلَمْ تُحِيطُوا بِهَا عِلْمًا أَمَّاذَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿86﴾ وَوَقَعَ الْقَوْلُ
عَلَيْهِم بِمَا ظَلَمُوا فَهُمْ لَا يَنطِقُونَ ﴿87﴾ أَلَمْ يَرَوْا أَنَّا جَعَلْنَا
الَّيْلَ لِيَسْكُنُوا فِيهِ وَالنَّهَارَ مُبْصِرًا إِنَّ فِي ذَٰلِكَ
لَءَايَاتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿88﴾ وَيَوْمَ يُنفَخُ فِي الصُّورِ فَفَزِعَ مَن
فِي السَّمَاوَاتِ وَمَن فِي الْأَرْضِ إِلَّا مَن شَاءَ اللَّهُ
وَكُلٌّ ءَاتُوهُ دَاخِرِينَ ﴿89﴾ وَتَرَى الْجِبَالَ
تَحْسِبُهَا جَامِدَةً وَهِيَ تَمُرُّ مَرَّ السَّحَابِ
صُنْعَ اللَّهِ الَّذِي أَتْقَنَ كُلَّ شَيْءٍ إِنَّهُ خَبِيرٌ بِمَا تَفْعَلُونَ ﴿90﴾

ربع

(WANI ABU NA DAGA ALAMOMIN TASHIN KIYAMA KAMAR RADIYO DA MAKAMANTANSU)

84. Idan maganar (azaba) ta auku a kansu (a cikin jimlar kafirai) sai mu fitar da dabbadaga garesu daga kasa, (wato gwamn falsafa,) [1] daza tayi zance dasu (da kowane harshe.) Hakika mutanen (Makka, daza a ce mutanen wannan zamanin) sun kasance basa sakankancewa da ayoyinmu (dayafi daccwa).Hakika kafiran Makka basu sakankance da ayoyinmu, wato Alkur'ani wanda ya knnshi tashin alkiyama da hisabi da ukuba, da fitowar ta ne Amri da ma'arufi zai yanke da hani ga barin aikin munkari tamfar da Allah ya aiko izuwa Annabi Nuhu. Hakika ba mai kuma gasgatawa daga mutanenka sai wadanda suka bada gaskiya.[2]

85. Ka ambata ranar da muke tarawa jama'a daga kowace al'umma daga wanda suke karyatawa da ayoyinmu (sune shiyagabanninmu ababan bi.) To, su ana tattara su a hadana karshen su izuwa na farkon su sannan a kora su.

86. Har idan sukazo gurin hisabi sai Ubangiji yace dasu "Shin kun karyata annabawana tareda ayoyina? Alhali baku kewaye ilimi da ita bana ja han karyatawar ku, ko Menene kuka kasance kuke aikatawa (daga abinda aka umarce ku?) [3]

87. Azabata tabbata a kansu, saboda sunyi shirka, to su bazasu iya. furuci da komai ba (don ba hujja a garesu.)

88. Shin basu san mun sanya dare mai duhu bane donsu nutsu a cikinsa (kamar waninsu). Mun sanya rana mai ganarwa (domin su ga juna a cikinsa domin su kai su kawo cikinsa) hakika akwai ayoyi (na ikon Allah) a cikin wancananka ga mutane masu bada gaskiya. (An kebance su da ambato saboda amfanuwarsu da ita a imani sabanin kafirai).

(BUSA KAHO WACCE TA KASU UKU TA GIRGIZA DATA MUTUWA DATA TASHI DAGA KABURBURA)

89. Ambaci ranar da ake yin busa (ta farko a cikin kaho daga Israfila alaihissalam, shi kahon na haske ne Allah ya halicce shi yaba Israfila shiya sanyashi a bakinsa ya daga kansa sama izuwa Al'arshi, yana sauraron yaushe za a umarce shi da busawa. Girman kowace kofa a cikinsa kamar fadin sama ne da kasa a cikinsa kamar yadda Sawi ya fada). Sai dukkan wanda yake cikin kasa yafirgita (firgitada zata kai izuwa mutuwa) sai wanda Allah ya toge, (Jibrilu da Mika'ilu da Israfilu Mala'ikan mutuwaIbn Abbasin yace sune masu mutuwar shahada donsu rayayyu ne nan ga Ubangijinsu.) Dukkan kowa zaizo masane yana wulakance.

(ISHARA IZUWA BAYYANAR JIRGIN SAMA)

90. Kana ganin duwarwatsu lokacin busa kana zaton ta sandararriya alhali tana wucewa irin wucewar girgije [3](idan iska ta bige shi tana tafiya har ta fado kanta har tayi daidai da ita, har ta zama kamar angalala sannan ta zama kura abar shekewa.) Allah ya aikata wannan aikatawa wandaya - kyautata kowane abu (daya halicce shi.) Hakika Ubangiji masanine da abinda kuke aikatawa. (FALALAR LA' ILAHA ILLALLAHU DA MAKAMANTANTA)

1) (BAYANI) (I) Alkur'ani mai girma wanda yakunshi dukkan ayoyin har izuwa tashin kiyama, bazai bar radiyo da makamantansu har izuwa tashin kiyama ba. In kuma akwai aya a cikin Alkur'ani wacce tayi nuni izuwa hikimar da talabijin da radiyo da maka-mantansu bazatafi wannan aya ba: (WA IZA WAKA'AL KAULU).Akwai hadisai wadanda ake rubutawa a wannan babi kamar jassasa, dabba mai binciken labari, Ni a ganina wannan dabba wacce take magana bazata wuce kafirin daya Rago talabijin da radiyo bada mak-amancinsu. Ubangiji yayi nuni da dabba a nan a kan mutum wato wanda ya kyautata ilimin kimiyyaya dandake falsafa har ya kai ga wadannan abubuwa, amma kasancewar-sa bai taba shakar kanshin Musulunci ba. Saboda haka Ubangiji bai ambace shi mutum ba bare mai ilimi To wadannan maganganu mun bayyanata anan amma mai duba yana cikin matukar 'yanci a kan ya karbako yabar min zancena. Allah ya sa mu dace, Amin. intaha 2) (BAYANI (II) Za tayi zance dasu ba sai lalle da dukkan harshe ba, ba sai lalle da Larabci ba tamfar dazai zama kamar shine ya tabbata. A tafsiri yace wannan magana ta dabba ce amma abindazai fi kyau ta zama maganar Allah ce. A cikin tafsiri yace, mutanen Makka, abinda yafi kyau a ce mutanen wannan lokaci basa sakankancewa da ayoyinmu, saboda su suna dogara da wannan aya ne izuwa dabbobin da suka Kage ta har, suna cewa Bature badama,! Bature ba kyau! Mai yiwuwa ne ya zama wannan magana tana nuna karshen abinda mutanen wannan lokaci zai kai izuwa gareshi) - Sanajiy -.

3) Wannan aya tana yin ishara da bayyar jirgin- sama Sabada bai zai yuwn ga mutum yaga yadda girgije yake gudu sai ko in yana cikin jirgin sana. Sanajiy

مَن جَآءَ بِالْحَسَنَةِ فَلَهُۥ خَيْرٌ مِّنْهَا وَهُم مِّن فَزَعٍ يَوْمَئِذٍ ءَامِنُونَ ﴿91﴾
وَمَن جَآءَ بِالسَّيِّئَةِ فَكُبَّتْ وُجُوهُهُمْ فِي النَّارِ هَلْ
تُجْزَوْنَ إِلَّا مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿92﴾ إِنَّمَآ أُمِرْتُ أَنْ أَعْبُدَ رَبَّ
هَٰذِهِ الْبَلْدَةِ الَّذِي حَرَّمَهَا وَلَهُۥ كُلُّ شَيْءٍ وَأُمِرْتُ أَنْ أَكُونَ مِنَ
الْمُسْلِمِينَ ﴿93﴾ وَأَنْ أَتْلُوَا الْقُرْءَانَ فَمَنِ اهْتَدَىٰ فَإِنَّمَا يَهْتَدِي
لِنَفْسِهِۦ وَمَن ضَلَّ فَقُلْ إِنَّمَآ أَنَا مِنَ الْمُنذِرِينَ ﴿94﴾ وَقُلِ الْحَمْدُ لِلَّهِ
سَيُرِيكُمْ ءَايَٰتِهِۦ فَتَعْرِفُونَهَا وَمَا رَبُّكَ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعْمَلُونَ ﴿95﴾

28 سُورَةُ الْقَصَصِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ ثَمَانٍ وَثَمَانُونَ ءَايَةً 88

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

* طسٓمٓ ﴿1﴾ تِلْكَ ءَايَٰتُ الْكِتَٰبِ الْمُبِينِ ﴿1﴾ نَتْلُواْ عَلَيْكَ مِن نَّبَإِ
مُوسَىٰ وَفِرْعَوْنَ بِالْحَقِّ لِقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿2﴾ إِنَّ فِرْعَوْنَ عَلَا فِي الْأَرْضِ
وَجَعَلَ أَهْلَهَا شِيَعًا يَسْتَضْعِفُ طَآئِفَةً مِّنْهُمْ يُذَبِّحُ أَبْنَآءَهُمْ
وَيَسْتَحْيِۦ نِسَآءَهُمْ إِنَّهُۥ كَانَ مِنَ الْمُفْسِدِينَ ﴿3﴾ وَنُرِيدُ أَن نَّمُنَّ عَلَى الَّذِينَ
اسْتُضْعِفُواْ فِي الْأَرْضِ وَنَجْعَلَهُمْ أَئِمَّةً وَنَجْعَلَهُمُ الْوَٰرِثِينَ ﴿4﴾

ثمن

91. Wanda yazoda hasana (wato La ilaha illallahu ranar alƙiyama) sakamako mafifici daga gare ta yana gareshi wanda yazo da ita, su amintattu ne daga firgicin barazana ta wannan rana.
92. Wanda yazoda sayyi'a (shirka) an kifar da fuskokinsu a cikin wuta, (wato fuskokinsu zata fada wuta, an ambaci fuska saboda ltace gurin daukaka daga sauran gabubba, waninta wanin fuskoki ('minbabi aula' ana gaya musu don katse hanzari). "Ba a saka muku sai sakamakon abinda kuka kasance kuna aikatawa (na shirka da sabon Allah".)

(GIR MANA MAKKA DA MAI SHE TA HARAMI DA KIRA IZUWA TILAWAR KUR'ANI DA GODE WA ALLAH)

93. Haƙiƙa an umarce ni in bautawa Ubangijin wannan gari (Makka) wanda yasanya taharumi ya amintac ce, (kada a zubar da jinin mutum a cikinta, ba a yankar ciyawarta, ba'a zaluntar kowa acikinta, ba'a farautar abin farautarta, wancananka yana daga ni'imomi a gurin Kuraishu a cikin daukewar azabada fitunu a garesu). Kowane abu mallakar Allah ne, an umarce ni in kasance daga cikin masu mika wuyaga Allah (da kadaita shi).
94. Kuma in karanta Alƙur'ani a gareku karatu na zuwa ga Allah da kira na imani, wanda ya shiriya to ya shiriya ne don kansa (domin ladan shiriyan nan nasa ne,) wanda ya bace ga barin shiriya, Yakuskure imani to, cene dashi dai hir, ni dai ina daga masu ban tsoro ne ba wani abu gareni illa isar da aike (wannan gaban umarnine da yaki.)
95. Cene, "Godiya ta tabbata ga Allah, da sannu zai nuna muku ayoyinsa ku san ta (sai Ubangiji ya nuna musu a ranar Badar, kisa da ribacewa da dukan Mala'iku fuskokinsu da bayayyakinsu yagag gautar dasu izuwa wuta.) Ubangijinka bai kasance marafkani ga barin abinda kuke aikatawa ba. (Yana jinkirta izuwa lokacin su kawai.)

Suratul ƙasasi

A Makka Aka. Saukar Da Ita Ayoyittta Tamanin Da takwas (88)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya mai jinƙan mumini a Lahira a keɓe

(WANNAN SURA TA MAKKACE TANA SANAR DA MUSULMI ZAMANIN DA MUSHIRIKAI AKE DANDANA MUSU AZABAR UKUBA CEWA NASARA DAGA ALLAH TAKE KUMA AMINCI YANA CIKIN MAKOTAKA DA ALLAH, KUMA CEWA KA-FIRAI YADDA DUK SUKA ƘASANCAE A ƘARFI DA ALFARMA DA DUKIYA RARSHENSU KISFEWA DA HALAKARWA, DON HAKA ALLAH YASANYA MISALI DA FIRAUNA DA ƘARUNA TAREDA AMBATON BA'ALIN MATSAYAI NA ALƘIYAMA)

1. D.S.M. (Allah masanine da abinda yake nufi da wancananka). Wannan ayoyi ayoyi ne na littafi mai bayyanarwar karya da gaskiya.
2. Muna labartawa gareka na daga labarin Annabi Musa da Fir'auna da gaskiya don mutane masu bada gaskiya (saboda sune masu amfani dashi).
3. Haƙiƙa Fir'auna yayi ginnan kai cikin birni n ƙasar Misra, yasanya mutane dabam-daban (a cikin hidimarsa) yana raunanar da waɗansu daga cikinsu (sune Banu-Isra'ila) yana yanyanka 'ya'yansu (ababan) haihuwa yana raya matayensu (saboda fadin ba'alin bokaye gareshi cewa wani abin haihuwa za a haife shi a cikin Banu Isra'ila zai kasarce sababin gushewar mulkinka). Haƙiƙa shi Fir'auna ya kasance daga cikakkur mabarnata (da kisa tsakaninsa).
4. Muna nufin mu yi baiwa ga waɗanda aka raunanar dasu a cikin ƙasa mu sanya su shiyagabanni (daza ayi koyi dasu a cikin alheri) Mun sanya su masu gadon (mulkin Fir'auna,) mun tabbatar dasu a cikin ƙasa (daga cikin asar Misra da Sham.

وَنُمَكِّنَ لَهُمْ فِي الْأَرْضِ وَنُرِيَ فِرْعَوْنَ وَهَامَانَ وَجُنُودَهُمَا
مِنْهُم مَّا كَانُوا يَحْذَرُونَ ﴿٥﴾ وَأَوْحَيْنَا إِلَىٰ أُمِّ مُوسَىٰ
أَنْ أَرْضِعِيهِ فَإِذَا خِفْتِ عَلَيْهِ فَأَلْقِيهِ فِي الْيَمِّ
وَلَا تَخَافِي وَلَا تَحْزَنِي إِنَّا رَادُّوهُ إِلَيْكِ وَجَاعِلُوهُ مِنَ الْمُرْسَلِينَ ﴿٦﴾
فَالْتَقَطَهُ آلُ فِرْعَوْنَ لِيَكُونَ لَهُمْ عَدُوًّا وَحَزَنًا
إِنَّ فِرْعَوْنَ وَهَامَانَ وَجُنُودَهُمَا كَانُوا خَاطِئِينَ ﴿٧﴾ وَقَالَتِ
امْرَأَتُ فِرْعَوْنَ قُرَّتُ عَيْنٍ لِّي وَلَكَ لَا تَقْتُلُوهُ عَسَىٰ أَن يَنفَعَنَا
أَوْ نَتَّخِذَهُ وَلَدًا وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿٨﴾ وَأَصْبَحَ فُؤَادُ أُمِّ مُوسَىٰ
فَارِغًا إِن كَادَتْ لَتُبْدِي بِهِ لَوْلَا أَن رَّبَطْنَا عَلَىٰ
قَلْبِهَا لِتَكُونَ مِنَ الْمُؤْمِنِينَ ﴿٩﴾ وَقَالَتْ لِأُخْتِهِ
قُصِّيهِ فَبَصُرَتْ بِهِ عَن جُنُبٍ وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿١٠﴾
۞ وَحَرَّمْنَا عَلَيْهِ الْمَرَاضِعَ مِن قَبْلُ فَقَالَتْ هَلْ أَدُلُّكُمْ ربع
عَلَىٰ أَهْلِ بَيْتٍ يَكْفُلُونَهُ لَكُمْ وَهُمْ لَهُ نَاصِحُونَ ﴿١١﴾
فَرَدَدْنَاهُ إِلَىٰ أُمِّهِ كَيْ تَقَرَّ عَيْنُهَا وَلَا تَحْزَنَ وَلِتَعْلَمَ
أَنَّ وَعْدَ اللَّهِ حَقٌّ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿١٢﴾

5. Mun tabbatar da mulkinsu a bayan ƙasa Mu nuna wa Fir'auna da (wazirinsa) Hamana da rundunarsu (daga cikin kasarsu abinda suka kasance suna tsoro (na daga abin haihuwar nan wandazai tafiyar da mulkinsa a bisa hannunsa. Ƙissar Annabi Musa alaihissalamu da haihuwarsa da sha dashi rono dal 145 rainonsa gidan Fir'auna da sababin fitarsa daga ƙasar Misra Izuwa kasar Madyana da saukar sa a kasar Madyana dasurkutarsa da ci kawarsa muddar jinga da zaza abin tsarkakewa da jayayyar Annabi Musa da taurin kan Fir'auna da aƙibarsu).
6. Muka aiko izuwa uwar Annabi Musa (wato jaririn da aka haifa wahayi na ilhami ba wanda yasan haihuwarsa sai 'yar uwarsa) cewa "shayar dashi mana . to idan kikaji tsoro a kansa, to ki jefa shi a cikin kogin Nil kada ki ji tsoron (nutsewarsa) kada kiyi bakin ciki (saboda rabuwa dashi), haƙiƙa Mu masu mayar dashine izuwa gare ki masu sanyashi cikin manzoninmune (ta shayar dashi wata uku, bayan kuwa ta ji tsoro a kansa ta ajiye shi cikin akwatu wanda aka shafe cikınsa da mangelo akayi masa shifida mai taushi, ta kulle shi ta jefa shi a kogin Nil da daddare).
7. Sai mataimakan Fir'auna suka tsince shi sundukin (saflyar wannan daren, ranar Litinin suka ajiye shi nan gaba gareshi, suka sanya Asiyatu ta bude shi bayan sun yi sun yi su bude sun kasa, aka fito da Annabi Musa daga cikinsa alhali shi yana tsotson nono daga babban yatsansa) don (a ƙarshe) ya kasance abokin gaba a garesu (wato Fir'auna da mutanensa, da kashe mazajensu) kuma da bakin ciki (wajen bautar da matayensu, haƙiƙa Fir'auna da Hamana da rundunarsu sun kasance masu kuskure (saboda haka akayi musu ukuba a hannun Annabi Musa alaihissalamu).
8. Matar Fir'auna (Asiyatu) Tace alhali shi da mutanensa sun yi nufin kashe Annabi Musa "Shi Annabi Musa sanyin idaniya ne a gareni dakai kadaku ,kashe shi, muna kaunar ya amfane mu, ko mu rike shi da". (Sai suka dakata alhali su basu san karshen al'amarinsu tare dashiba.
9. Zuciyar uwar Annabi Musa ta zama ta wayi gari mawofanciyaga komai (sai shi, yayin da tayi sanyi da tsintar sa, haƙiƙa ita dai uwar Annabi Musa) ta kusa ta bayyana dashi da cewa danta ne ba don munyi dauri a kan zuciyarta ba (da hakuri) donta kasance daga muminai (masu gasgatawa da alkawarin Allah.)
10. Tace da 'yar uwarta (Maryamu) "Bi sawunsa (har ki samo labarinsa") saita hango shi daga nesa a fizge alhali su basu san (cewa ita 'yar uwarsa ce bakuma cewa ita tana la'akarinsa ba.
11. Mun haramta masa masu sha da nono tun gaban (mayar dashi izuwa mahaifiyarsa bai karɓi nononsu ba sai uwarsa, 'yar uwarsa tace, "Shin bana shiryar daku ,a bisa mutanen gida ba, (wato yayin data ga jinkansu a gareshi shine Tace bana shiryar daku ,bisa mutanen gida) daza suyi muku rainon sa? ba Alhali su masu nasiha ne a gareshi (sai aka amsa mata, saita zoda uwarsa, saiya kama nononta, sukace me ya sa ya karbi nononta? Saitace dasu saboda daɗin ƙanshin jikintada daɗin nononta, sai akayi mata izini ta tafi dashi gadonta ta shayar dashi a gidanta a ɗakinta, to saita koma dashi tamfar da Ubangiji yace Subhanahu Wata'ala).
12. Sai muka mai dashi izuwa mahaifiyarsa don idaniyarta tayi sanyi da saduwa dashi, baza tayi bakin ciki ba a yayin nan kiima donta sani alƙawarin Allah da mai dashi gareta gaskiya ne, sai dai yawancin mutane basu san (wannan alkawari ba basu san wannan yar uwarsa ce ba, basu san wannan uwarsa ce ba. Ya zauna gurinta har izuwa ta yaye shi aka bata ladanta kowane wuni dinare daya. Ta karbi wannan kudi saboda cewa wannan kudi ɗukiyar kafirin yaki ce ta kai wa Fir'auna shiya rainu nan gareshi kamar yadda Ubangiji ta'ala ya fada don faɗakarwa a gareshi a cikin Suratul Shu'ara'i, Shin bamu raine ka a cikinmu kana yaro ba har Izuwa karshe)

وَلَمَّا بَلَغَ أَشُدَّهُۥ وَاسْتَوَىٰٓ ءَاتَيْنَٰهُ حُكْماً وَعِلْماًۖ
وَكَذَٰلِكَ نَجْزِے اِ۬لْمُحْسِنِينَ ﴿13﴾ وَدَخَلَ اَ۬لْمَدِينَةَ عَلَيٰ حِينِ غَفْلَةٖ مِّنْ أَهْلِهَا
فَوَجَدَ فِيهَا رَجُلَيْنِ يَقْتَتِلَٰنِ هَٰذَا مِن شِيعَتِهِۦ وَهَٰذَا مِنْ عَدُوِّهِۦۖ
فَاسْتَغَٰثَهُ اُ۬لذِے مِن شِيعَتِهِۦ عَلَى اَ۬لذِے مِنْ عَدُوِّهِۦ
فَوَكَزَهُۥ مُوسَيٰ فَقَضَيٰ عَلَيْهِۖ قَالَ هَٰذَا مِنْ عَمَلِ اِ۬لشَّيْطَٰنِۖ
إِنَّهُۥ عَدُوّٞ مُّضِلّٞ مُّبِينٞۖ ﴿14﴾ قَالَ رَبِّ إِنِّے ظَلَمْتُ نَفْسِے فَاغْفِرْ لِے فَغَفَرَ لَهُۥٓۖ
إِنَّهُۥ هُوَ اَ۬لْغَفُورُ اُ۬لرَّحِيمُۖ ﴿15﴾ قَالَ رَبِّ بِمَآ أَنْعَمْتَ عَلَيَّ فَلَنْ أَكُونَ ظَهِيراً
لِّلْمُجْرِمِينَۖ ﴿16﴾ فَأَصْبَحَ فِے اِ۬لْمَدِينَةِ خَآئِفاً يَتَرَقَّبُ فَإِذَا اَ۬لذِے
اِ۪سْتَنصَرَهُۥ بِالْأَمْسِ يَسْتَصْرِخُهُۥۖ قَالَ لَهُۥ مُوسَيٰٓ إِنَّكَ لَغَوِيّٞ مُّبِينٞۖ ﴿17﴾
فَلَمَّآ أَنْ أَرَادَ أَنْ يَّبْطِشَ بِالذِے هُوَ عَدُوّٞ لَّهُمَا قَالَ يَٰمُوسَيٰٓ
أَتُرِيدُ أَن تَقْتُلَنِے كَمَا قَتَلْتَ نَفْساَۢ بِالْأَمْسِۖ إِن تُرِيدُ إِلَّآ أَن
تَكُونَ جَبَّاراً فِے اِ۬لْأَرْضِ وَمَا تُرِيدُ أَن تَكُونَ مِنَ اَ۬لْمُصْلِحِينَۖ ﴿18﴾
۞ وَجَآءَ رَجُلٞ مِّنْ أَقْصَا اَ۬لْمَدِينَةِ يَسْعَيٰۖ قَالَ يَٰمُوسَيٰٓ إِنَّ اَ۬لْمَلَأَ
يَأْتَمِرُونَ بِكَ لِيَقْتُلُوكَ فَاخْرُجْ إِنِّے لَكَ مِنَ اَ۬لنَّٰصِحِينَۖ ﴿19﴾
فَخَرَجَ مِنْهَا خَآئِفاً يَتَرَقَّبُۖ قَالَ رَبِّ نَجِّنِے مِنَ اَ۬لْقَوْمِ اِ۬لظَّٰلِمِينَۖ ﴿20﴾

ثمن

13. Yayin daya isa ganiyar sa (ya cika barnarsa shine ya isa shekara arba'in) sai muka bashi hikima da fahinta (a cikin addini tun ba a aiko shi annabi ba) kamar yadda muka saka masa muke saka wa masu kyakkyawan aiki (ga kawunansu)

(SHIGAR SA MUNFU BIRNIN FIR'AUNA)

14. Annabi Musa (alaihissalatu wassalamu) ya shiga birnin (Fir'auna, Munfu, bayan ya faku ga barin sa zamani mai tsaho) a bisa zamanin gafala ta mutanen ta (zamanin barcin rana) saiya sami mutun biyu a cikinta suna fada, wannan na daga kabilarsa (Ba'isra'ile) wannan daga magaucinsa (Bakibđe yana wahalar da Ba'isra'ile donya dora masa kayan icce izuwa madafar Fir'auna) sai Ba'isra'ile wanda yake daga cikin kabilarsa ya nemi taimakonsa a kan wanda yake daga magautansa Bakibđe, (sai Annabi Musa yace dashi bar shiya wuce Ance hakika shi yace da Annabi Musa lalle ni nayi niyya na đora shi a kanka, nayi nufin in đora Itacen a kanka) sai Annabi Musa ya naushe shi (shi kuwa Annabi Musa mai tsananin karfi ne mai rikon tsauri) saiya kashe shi (ba tare dayanufi kashe shi baya binne shi a cikin rairayi) yace "Wannan aikin kisan nan daga aikin shaiđan ne (wanda ya motso fushina) hakika shi shaiđan magauci ne ga dan Adam mai ɓatarwa ne gareshi mabayyanin (ɓatarwa, ya fadayana mai nadama.)

15. Yace, "Ubangijina, ni na zalunci kaina, kayi gafara gare ni, saiya gafarta masa, hakika shine mai yawan gafara mai yawan jinkai (tun fil'azal kuma har abada").

16. Yace, "Ubangijina saboda girman ni'imtawar da kayi min da gafara, kiyaye ni kada in zamo mai taimako ga kafirai ba (har abada to wannan in ka kiyaye nine zan sami haka").

17. Ya wayi gari a cikin wannan gari Munfa yana sauraron abindazai sameshi na dagga wannan kasasshe, sai ga wanda ya nemi taimakonsa ajiya yana neman taimakonsa a kan wani Bakibden daban, sai Annabi Musa yace masa "Hakika kai halakakkene, ma bai yanin halaka, saboda abinda ka aikata jiya dayau".

18. Yayin dayanufi yai danka ga wandashi magauci ne nasu gabadaya wato shi Annabi Musa da wanda yake neman taimako dashi, mai neman taimakon nan yace yana mai zaton shi zai rike shi sai yace dashi "Ya Musa kana nufin ka kashe nine kamar yadda kayi kisan kai a jiya, kana nufin ka zama jabberi ne a cikin kasa?" Baka nufin komai sai jabberanci a cikin kasa. Sai Bakibđe nan yaji wannan sai yasan cewa dai mai kisan nan dai Annabi Musa ne, saiya tafi (zuwa Fir'auna ya bashi labari daga gareshi sai Fir'auna ya umarci haunaye wato masu yanka mutane da kashe Annabi Musa,

19. Sai wani mutum yazo shine muminin ali Fir'auna daga mafi nisan gari wato karshen gari yana gaggawa a cikin tafiyarsa ga hanya mafi kusa a gareshi wato gajeriyar hanya yace Ya Musa mutanen Fir'auna suna shawara a kanka donsu kashe ka, fita daga wannan gare hakika ni, mai nasiha ne gari ka a cikin umarni da fita.

20. Sai yafita daga gare ta yana mai tsoro yana sauraron taimakon Allah, yace Ubangiji tserar dani daga mutane azzalumai (wato mutanen Fir'auna).

وَلَمَّا تَوَجَّهَ تِلْقَآءَ مَدْيَنَ قَالَ عَسيٰ رَبِّيَ أَن يَّهْدِيَنِي سَوَآءَ اَلسَّبِيلِ ﴿21﴾
وَلَمَّا وَرَدَ مَآءَ مَدْيَنَ وَجَدَ عَلَيْهِ أُمَّةً مِّنَ اَلنَّاسِ يَسْقُونَ ﴿22﴾
وَوَجَدَ مِن دُونِهِمُ اُمْرَأَتَيْنِ تَذُودَانِ قَالَ مَا خَطْبُكُمَا
قَالَتَا لَا نَسْقِي حَتَّيٰ يُصْدِرَ اَلرِّعَآءُ وَأَبُونَا شَيْخٌ كَبِيرٌ ﴿23﴾ فَسَقيٰ
لَهُمَا ثُمَّ تَوَلَّيٰ إِلَى اَلظِّلِّ فَقَالَ رَبِّ إِنِّي لِمَا أَنزَلْتَ إِلَيَّ مِنْ
خَيْرٍ فَقِيرٌ ﴿24﴾ فَجَآءَتْهُ إِحْدَيٰهُمَا تَمْشِي عَلَى اَسْتِحْيَآءٍ
قَالَتِ إِنَّ أَبِي يَدْعُوكَ لِيَجْزِيَكَ أَجْرَ مَا سَقَيْتَ لَنَا
فَلَمَّا جَآءَهُۥ وَقَصَّ عَلَيْهِ اِلْقَصَصَ قَالَ لَا تَخَفْ نَجَوْتَ مِنَ
اَلْقَوْمِ اِلظَّٰلِمِينَ ﴿25﴾ قَالَتِ إِحْدَيٰهُمَا يَٰأَبَتِ اِسْتَأْجِرْهُ
إِنَّ خَيْرَ مَنِ اِسْتَأْجَرْتَ اَلْقَوِيُّ اُلْأَمِينُ ﴿26﴾ قَالَ إِنِّيَ أُرِيدُ
أَنُ اُنكِحَكَ إِحْدَى اَبْنَتَيَّ هَٰتَيْنِ عَلَيٰ أَن تَأْجُرَنِي ثَمَٰنِيَ حِجَجٍ
فَإِنْ أَتْمَمْتَ عَشْراً فَمِنْ عِندِكَ وَمَا أُرِيدُ أَنَ اَشُقَّ عَلَيْكَ
سَتَجِدُنِي إِن شَآءَ اَللَّهُ مِنَ اَلصَّٰلِحِينَ ﴿27﴾ قَالَ
ذَٰلِكَ بَيْنِي وَبَيْنَكَ أَيَّمَا اَلْأَجَلَيْنِ قَضَيْتُ
فَلَا عُدْوَٰنَ عَلَيَّ وَاللَّهُ عَلَيٰ مَا نَقُولُ وَكِيلٌ ﴿28﴾

(SHIGAR ANNABI MUSA MADYANA DASURKUTARSA DA ANNABI SHU'AIBU)

21. Yayin daya fuskanci (katar nin) Madyana (jiharta, Itace alkaryar Annabi Sha'aibu alaihissalamu tafiyar kwana takwas ne daga Misra, an ambace ta dasunan Madyana dasunan dan Annabi Ibrahim alaihissalamu, bai san hanyarta baya fuskance ta ne da ilhama daga Ubangiji) sai yace ina kaunar Ubangijina ya shirye ni tafarki madaidaici izuwa gare ta sai (Allah saiya aiko masa Mala'ika, akwai dan karamin mashi a hannunsa sai ya
22. (Zamanin daya je ruwan Madayana wato rijiyar) saiya sami al'uma da yawa a kan ruwan rijiyar daga mutane suna shayar da dabbobinsu.
23. Ya sami wadansu mataye wato koma-bayansu suna hana dabbobinsu ga barin shayuwa (sai Annabi Musa yace Menene sha'aninkune ba kwa shayar da ruwa ga dabbobi? Sai sukace Barna shayarwa har sai makiyaya sun komo ga barin shayarwarsu don tsoron matsatsi, sai mu shayar a sannan) har sai makiyaya sun kore dabbobinsu ga barin ruwa, mahaifinsu kuma tsoho ne babba bashi da iko ya shayar. Ya rayu shekara dubu uku (3,000) ko dubu hudu (4,000).
24. To, saiya shayar garesu (daga wata rijiyar da take kusa dasu ya dauke dutse ga barin ta wanda ba mai iya dauke shi sai mutum goma) sannan ya juya izuwa inuwar farar kaya saboda tsananin zafin rana alhali shi kuma yana jin yunwa) sai yace Ya Ubangijina, Ni mabukaci ne izuwa ga abinda ka saukar gareni (wato abinci). (Suka koma izuwa mahaifinsu a zamani mafi karanci kamar yadda suka saba komawa a cikinsa, saiya tambaye su da wancananka sai suka bashi labari ga wanda ya shayar dasu sai yace da dayansu kirawo shi yazo guna, sai Ubangiji yace;
25. Sai dayar su tazo tana tafe a cikin kunya (wato ta ajiye hannun rigarta a kan fuskarta don kunyarsa) Tace babana hakika yana kiranka donya saka maka ladan shayarwar da kayi mana (saiya amsa mata yana mai musun karbar ladan a cikin zuciyarsa kamar (ita tana nufin sakayya ne in ya kasance daga wadanda suke nufin sakayyar). Saita shige gaba gareshi sai iska ta hadu tana dukan fuskarta saita yaye mata makyangyamarta sai yace da ita biyo bayana ki shiryar dani a kan hanya, to saita aikata har izuwa mahaifinta shine Annabi Shu'aibu (alaihissalamu) (akwai abincin dare gurinsa sai yace dashi zauna mu ci abinci, sai yace ina tsoron kada ya zama ladan shayarwar da nayi musu, mu mutanen gida ne wanda Barna neman lada bisa aiki, sai Annabi Shu'aibu yace a'a, al'adata data iyayena ciyar da baki da raba abinci saiya ci) saiya bashi labari da halin da yake ciki. Sai Ubangiji yace, Yayin dayazomasa ya labarta masa halin da yake ciki (na kisan Bakibde da nufin su kashe shi da tsoronsa daga Fir'auna) yace kada kaji tsoro ka tsira daga mutane azzalumai (saboda Fir'auna bashi da hannu a kan Madyana).
26. Sai dayar su babbar ko kanwar wadda Annabi Musa (alaihissalamu) ya aura, Tace ya babana rike shi abin sufurta yayi kiwon tumakai maimakon mu, hakika mafificin wanda zaka sifirce shi kakkarfa amintacce (sifirce shi saboda karfin sa da amanarsa, saiya tambaye ta ga karfin sa da amanarsa, saiya tambaye ta ga karfin da amanar, saita bashi labari da abinda yagabata na daga daukewar sa dutse kan rijiya da fadin sa ki tafi a bayana kuma da karin hakika cewa ita yayin datazo masa ya sami sani da ita saiya sunkuyar da wuyansa bai dagashi sama ba, sai yayi kwadayi a cikin aurenta).
27. Yace, "Hakika ni ina nufin in aura maka dayar 'ya'yan nan nawa guda biyu mata (yar ko kanwar) a bisa ka zama dan sifirina (a cikin kiwon dabbobina) a shekara takwas in ka cika goma to, wannan daga gareka ne bana nufin in wahalar dakai (da shardanta goma) da sannu zaka same ni in sha -allahu daga cikin managarta (nagari)".
28. Sai Annabi Musa yace wancananka (wato abinda na fade shi,) tsakanina dakai kowanne daga abin nan guda biyu na takwas ko goma babu wani kari a ciki na neman kari. Ubangiji shine wakili a bisa abinda muke fada (ni dakai sai kulle ya shiga da fadar wannan maganar, Annabi Shu'aibu ya umarci 'yarsa ta ba Annabi Musa sanda dazai dinga kora namun daji da ita ga barin tumakansa sandunan Annabawa sun kasance nan ga Annabi =

ربع

* فَلَمَّا قَضَىٰ مُوسَى ٱلْأَجَلَ وَسَارَ بِأَهْلِهِۦٓ ءَانَسَ مِن جَانِبِ ٱلطُّورِ نَارًا
قَالَ لِأَهْلِهِ ٱمْكُثُوٓا۟ إِنِّىٓ ءَانَسْتُ نَارًا لَّعَلِّىٓ ءَاتِيكُم
مِّنْهَا بِخَبَرٍ أَوْ جِذْوَةٍ مِّنَ ٱلنَّارِ لَعَلَّكُمْ تَصْطَلُونَ ﴿29﴾
فَلَمَّآ أَتَىٰهَا نُودِىَ مِن شَٰطِئِ ٱلْوَادِ ٱلْأَيْمَنِ فِى ٱلْبُقْعَةِ
ٱلْمُبَٰرَكَةِ مِنَ ٱلشَّجَرَةِ أَن يَٰمُوسَىٰٓ إِنِّىٓ أَنَا ٱللَّهُ رَبُّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿30﴾
وَأَنْ أَلْقِ عَصَاكَ ۖ فَلَمَّا رَءَاهَا تَهْتَزُّ كَأَنَّهَا جَآنٌّ وَلَّىٰ مُدْبِرًا
وَلَمْ يُعَقِّبْ ۚ يَٰمُوسَىٰٓ أَقْبِلْ وَلَا تَخَفْ ۖ إِنَّكَ مِنَ ٱلْءَامِنِينَ ﴿31﴾
ٱسْلُكْ يَدَكَ فِى جَيْبِكَ تَخْرُجْ بَيْضَآءَ مِنْ غَيْرِ سُوٓءٍ وَٱضْمُمْ إِلَيْكَ
جَنَاحَكَ مِنَ ٱلرَّهْبِ ۖ فَذَٰنِكَ بُرْهَٰنَانِ مِن رَّبِّكَ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ
وَمَلَإِي۟هِۦٓ ۚ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ قَوْمًا فَٰسِقِينَ ﴿32﴾ قَالَ رَبِّ إِنِّى قَتَلْتُ
مِنْهُمْ نَفْسًا فَأَخَافُ أَن يَقْتُلُونِ ﴿33﴾ وَأَخِى هَٰرُونُ هُوَ
أَفْصَحُ مِنِّى لِسَانًا فَأَرْسِلْهُ مَعِىَ رِدًا يُصَدِّقُنِىٓ ۖ إِنِّىٓ
أَخَافُ أَن يُكَذِّبُونِ ﴿34﴾ قَالَ سَنَشُدُّ عَضُدَكَ
بِأَخِيكَ وَنَجْعَلُ لَكُمَا سُلْطَٰنًا فَلَا يَصِلُونَ إِلَيْكُمَا
بِـَٔايَٰتِنَآ ۚ أَنتُمَا وَمَنِ ٱتَّبَعَكُمَا ٱلْغَٰلِبُونَ ﴿35﴾

Shu'aibu (alaihissalamu) sai sandar Annabi Adamu ta fada hannun ta sai Annabi Musa ya karbe tada izinin Annabi Shu'aibu) Ha sandarta, asuce na aljanna.

29. Yayin da Annabi Musa ya cika wannan alkawari na shekara goma ya tafi da iyalinsa wato matarsa (da izinin ubanta izuwa Misra) to sai daga nesa yagano nahiyar wuta yace da iyalinsa ku zauna (a nan) ni na gano wuta saboda watakila nazo mukuda labarin (hanyaya kasance ya bace) ko dosanan wuta, wata kila kwa ji dumi.)

30. Yayin dayazowa wutar nan sai akayi kira ta nahiyar zaza na dama da (annabi Musa) a gud mai albarka na guri mai girma (saboda yaji zancen Ubangijinsa nan ga itaciyar, (wato ita itaciyar kayace ta nama-nama ko wutar dundu, cewa Musa Nine Allah mana llakin talikai.

(ANNABI MUSA ALAIHISSALAMU YAGAMA MUDDAR ADADIN KIWO YA SHIGA TAFIYA A CIKIN WADIN MUƘADDASU)

31. Aka kira shiya Musa cewa yada sandarka, yayin dayaganta tana wuwul-wuwul kai kace ita macijiyace karama saiya tsinka aguje (yana gudunta) bai juyo da bayaba sai aka kira shiya Musa gabato kada kaji tsoro, haƙiƙa kai kana daga cikin amintattu,

32. "Shigar da tafin hannunka na dama cikin wuyan rigarka ka fitar da ita ta fito fara fata ba tareda wani laifi (na baras ba, saiya shigar da hannunsa kuma ya zaro ta tana haske kamar kyalkyalin rana, tana dusashe ido) ka tara hannunka izuwa hannunka ta hagun saboda tsoro (wanda ya faru saboda hasken hannun wato ka shigar da ita a cikin wuyar rigarka saboda da ita a cikin wuyar rigarka sabodata koma izuwa halinta na farko don tsoron da kaji ya kau.) Wancananka guda biyu (sanda da hannu) hujja ce guda biyu daga Ubangijinku izuwa Fir'auna da manyan mutanensa, haƙiƙa su sun kasance mutane fasiƙai".

33. Yace, "Ubangiji, haƙiƙa ni nayi kisan kai na Baƙibɗe ina jin tsoron su kashe ni (maimakonsa).

34. "Dan'uwana Harunu shine mafi fasahar (harshe) daga gare ni, Ya Ubangiji aiko shiya sadu dani yana mai taimako yagasgata ni, haƙiƙa ni inajin tsoro su karyata ni!"

35. Yace, "Da sannu zamu ƙarfafa dantsenka da dan uwanka mu sanya muku rinjaye (kai dashi) basa sadu izuwa gareka da mummuna ba, ku je da ayoyina kuda wanda yabi ku kune masu rinjaye (a kansu!")

فَلَمَّا جَآءَهُم مُّوسَىٰ بِـَٔايَـٰتِنَا بَيِّنَـٰتٍ قَالُواْ مَا هَـٰذَآ إِلَّا
سِحْرٌ مُّفْتَرًى وَمَا سَمِعْنَا بِهَـٰذَا فِيٓ ءَابَآئِنَا ٱلْأَوَّلِينَ ﴿36﴾
وَقَالَ مُوسَىٰ رَبِّيٓ أَعْلَمُ بِمَن جَآءَ بِٱلْهُدَىٰ مِنْ عِندِهِۦ
وَمَن تَكُونُ لَهُۥ عَـٰقِبَةُ ٱلدَّارِ إِنَّهُۥ لَا يُفْلِحُ ٱلظَّـٰلِمُونَ ﴿37﴾
ثمن
۞ وَقَالَ فِرْعَوْنُ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلْمَلَأُ مَا عَلِمْتُ لَكُم مِّنْ إِلَـٰهٍ غَيْرِي
فَأَوْقِدْ لِي يَـٰهَـٰمَـٰنُ عَلَى ٱلطِّينِ فَٱجْعَل لِّي صَرْحًا لَّعَلِّيٓ
أَطَّلِعُ إِلَىٰٓ إِلَـٰهِ مُوسَىٰ وَإِنِّي لَأَظُنُّهُۥ مِنَ ٱلْكَـٰذِبِينَ ﴿38﴾
وَٱسْتَكْبَرَ هُوَ وَجُنُودُهُۥ فِي ٱلْأَرْضِ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ وَظَنُّوٓاْ
أَنَّهُمْ إِلَيْنَا لَا يُرْجَعُونَ ﴿39﴾ فَأَخَذْنَـٰهُ وَجُنُودَهُۥ فَنَبَذْنَـٰهُمْ
فِي ٱلْيَمِّ فَٱنظُرْ كَيْفَ كَانَ عَـٰقِبَةُ ٱلظَّـٰلِمِينَ ﴿40﴾
وَجَعَلْنَـٰهُمْ أَئِمَّةً يَدْعُونَ إِلَى ٱلنَّارِ وَيَوْمَ ٱلْقِيَـٰمَةِ
لَا يُنصَرُونَ ﴿41﴾ وَأَتْبَعْنَـٰهُمْ فِي هَـٰذِهِ ٱلدُّنْيَا لَعْنَةً
وَيَوْمَ ٱلْقِيَـٰمَةِ هُم مِّنَ ٱلْمَقْبُوحِينَ ﴿42﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَى
ٱلْكِتَـٰبَ مِنۢ بَعْدِ مَآ أَهْلَكْنَا ٱلْقُرُونَ ٱلْأُولَىٰ بَصَآئِرَ
لِلنَّاسِ وَهُدًى وَرَحْمَةً لَّعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿43﴾

(JAYAYYAR FIR'AUNA GA ANNABI MUSA DA MUTANENSA DA TAU-RIN- KANSU GARESHI)

36. Yayin da Annabi Musa yazo mana da ayoyinmu mabayyana sai Sukace, "Wannan bai kasance ba sai tsafi abin ƙirƙira, bamu taɓa jin irin wannan a cikin kwanikan iyayenmu na farko ba".
37. Annabi Musa yace, "Ubangijina ne masani da wanda yazo dashiriyagareshi da wanda kyak-kyawan karshe a lahira ta kasance a gareshi, haƙiƙa kafirai azzalumai bazasu tsira ba".
38. Fir'auna yace, "Yaku manyan jama'ata ni ban san wani Ubangiji gareku bani ba, ku hura min wuta kan yunbu, ya Hamana ka sanya min soron bene saboda in tsinkaye izuwa Ubangijin Annabi Musa, haƙiƙa ni lalle inazaton sa cikin maƙaryata (a cikin da'awarsa wani ubangiji daban da kuma cewa shi manzon Allah ne.")
39. Fir'auna yayi girman kai shi da rundunarsa a ƙasar (Misra) bada gaskiya ba, sun zaci haƙiƙa su bazasu komo izuwa garemu ba.
40. Sai muka rike shi da rindinarsa muka jefa su a cikin kogin ruwan Maliya, kayi dubaka gane yaya karshen azzalumai ya kasance?
41. Mun sanya su shiyagabanni a duniya dasuke kira izuwa wuta (kiransu izuwa shirka) ranar Lahira baza a ije musu azaba ba.
42. Mun biyar musu da tsinewar albarka a wannan duniya (wato kunyata,) a ranar Lahira su suna daga ababan nisantawa daga rahamar Ubangiji.
43. Haƙiƙa mun baiwa Annabi Musa Attaura bayan mun halakar da tsareku na farko (mutanen Annabi Nuhu da Adu da Samudu da waninsu.) Ma'abocin basirori ga mutane, shiriya (daga bata ga wanda yayi aiki dashi) kuma rahama (ga wanda ya bada gaskiya dashi wata kila sa bi Allah,) saboda ana tabbata kaunar sa wa'azantu.

وَمَا كُنتَ بِجَانِبِ ٱلْغَرْبِيِّ إِذْ قَضَيْنَآ إِلَىٰ مُوسَى ٱلْأَمْرَ
وَمَا كُنتَ مِنَ ٱلشَّٰهِدِينَ ﴿44﴾ وَلَٰكِنَّآ أَنشَأْنَا قُرُونًا
فَتَطَاوَلَ عَلَيْهِمُ ٱلْعُمُرُ وَمَا كُنتَ ثَاوِيًا فِىٓ أَهْلِ مَدْيَنَ
تَتْلُوا۟ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتِنَا وَلَٰكِنَّا كُنَّا مُرْسِلِينَ ﴿45﴾
وَمَا كُنتَ بِجَانِبِ ٱلطُّورِ إِذْ نَادَيْنَا وَلَٰكِن رَّحْمَةً مِّن رَّبِّكَ
لِتُنذِرَ قَوْمًا مَّآ أَتَىٰهُم مِّن نَّذِيرٍ مِّن قَبْلِكَ لَعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿46﴾
وَلَوْلَآ أَن تُصِيبَهُم مُّصِيبَةٌۢ بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ فَيَقُولُوا۟
رَبَّنَا لَوْلَآ أَرْسَلْتَ إِلَيْنَا رَسُولًا فَنَتَّبِعَ ءَايَٰتِكَ وَنَكُونَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿47﴾
فَلَمَّا جَآءَهُمُ ٱلْحَقُّ مِنْ عِندِنَا قَالُوا۟ لَوْلَآ أُوتِىَ مِثْلَ مَآ أُوتِىَ
مُوسَىٰٓ ۚ أَوَلَمْ يَكْفُرُوا۟ بِمَآ أُوتِىَ مُوسَىٰ مِن قَبْلُ ۖ قَالُوا۟ سِحْرَانِ
تَظَٰهَرَا وَقَالُوٓا۟ إِنَّا بِكُلٍّ كَٰفِرُونَ ﴿48﴾ قُلْ فَأْتُوا۟ بِكِتَٰبٍ
مِّنْ عِندِ ٱللَّهِ هُوَ أَهْدَىٰ مِنْهُمَآ أَتَّبِعْهُ إِن كُنتُمْ
صَٰدِقِينَ ﴿49﴾ فَإِن لَّمْ يَسْتَجِيبُوا۟ لَكَ فَٱعْلَمْ أَنَّمَا يَتَّبِعُونَ
أَهْوَآءَهُمْ ۚ وَمَنْ أَضَلُّ مِمَّنِ ٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ بِغَيْرِ هُدًى
مِّنَ ٱللَّهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿50﴾

(BUKATUWAR AL'UMMA IZUWA AIKO MANZANNI TAREDA BA'ALIN DALILAI A KAN WANZUWAR MANZO)

44. Baka kasance ajanibi a gefen dutse ko zaza na yamma badaga janibin Annabi Musa yayin ganawa,) yayin da muka aiko risala izuwa annabi Musa (da aka aiko shi izuwa Fir'auna da mutanensa) baka kasance cikin masu halarta (ga wancananka ba, bare kasanshi ka labarta dashi).
45. Sai dai mu mun fari tsarekune (wato al'ummatai bayan Annabi Musa) baka kasance mazauni a cikin jama'ar Madyana kana karantawar ayoyinmu a garesu ba, (bare kasan labarinsu ka labarta dashi) sai dai mu, mune muka tabbata masu aikowa (gareka ga labarin magabata).
46. Baka kasance a gefen dutse bazamanin da muka kira (Annabi Musa mu kace dashiya riƙi littafi da ƙarfi) sai dai mun aiko ka don rahama daga Ubangijinka domin ka tsoratar da mutanen da wani mai gargaɗi gabanka bai zo mu su ba, (sune mutanen Makka) saboda kaunar ta su wa'azantu.

(MUMINAI DAGA MAZOWA LITTAFI)

47. Ba don gudun kada uƙubata samesu saboda abinda hannuwansu ta gabatar (na kafirci da waninsa) su ce ya "Ubangijinmu donme baka aiko manzo izuwa garemu bamu bi ayoyinka mu kasance daga muminai" (da mun gaggauta musu ukuba, kuma da bamu aiko musu da manzo ba).
48. Yayin da manzon Allah (S.A.W) yazo musu da gaskiya daga garemu sai sukace "Donme ba a bashi irin abinda aka baiwa Annabi Musa ba? (Na daga ayoyi, kamar hannu fari da sanda da littafi gabadaya da makamancinsu", Ubangiji yace,) "Shin basu kafirce da abinda aka ba wa Annabi Musa din bane tun gabansa? Yayin da sukace (a cikin Annabi Musa da Annabi Muhammadu) "matsafa ne guda biyu (kuma sukace Alƙur'an da Attaura tsafi ne) su matsafan nan guda biyu da suka taimaki juna suka. ce, " Haƙiƙa mu mun kafirce da dukkansu (wato Annabawan guda biyu da littattafan guda biyu").
49. Cene (dasu) "To ku zoda littafi daga Allah wanda yafi shiryarwa daga garesu in bi shi in kun kasance magasgata a cikin maganarku.
50. To, in basu zo maka da wannan littafin ba to, ka sani haƙiƙa suna bin soye-soyen zukatansune kawai a cikin kafircinsu, waye mafi bata daga wanda yabi son zuciyarsa badashiriya daga Allah ba? Ba mafi bata daga gareshi. Haƙiƙa Ubangiji baya shiriyar mutane kafirai.

حزب

* وَلَقَدْ وَصَّلْنَا لَهُمُ ٱلْقَوْلَ لَعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿51﴾ ٱلَّذِينَ
ءَاتَيْنَٰهُمُ ٱلْكِتَٰبَ مِن قَبْلِهِۦ هُم بِهِۦ يُؤْمِنُونَ ﴿52﴾ وَإِذَا يُتْلَىٰ
عَلَيْهِمْ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا بِهِۦٓ إِنَّهُ ٱلْحَقُّ مِن رَّبِّنَآ إِنَّا كُنَّا
مِن قَبْلِهِۦ مُسْلِمِينَ ﴿53﴾ أُوْلَٰٓئِكَ يُؤْتَوْنَ أَجْرَهُم مَّرَّتَيْنِ
بِمَا صَبَرُواْ وَيَدْرَءُونَ بِٱلْحَسَنَةِ ٱلسَّيِّئَةَ وَمِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ
يُنفِقُونَ ﴿54﴾ وَإِذَا سَمِعُواْ ٱللَّغْوَ أَعْرَضُواْ عَنْهُ وَقَالُواْ لَنَآ
أَعْمَٰلُنَا وَلَكُمْ أَعْمَٰلُكُمْ سَلَٰمٌ عَلَيْكُمْ لَا نَبْتَغِي ٱلْجَٰهِلِينَ ﴿55﴾
إِنَّكَ لَا تَهْدِي مَنْ أَحْبَبْتَ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَهْدِي مَن يَشَآءُ
وَهُوَ أَعْلَمُ بِٱلْمُهْتَدِينَ ﴿56﴾ وَقَالُوٓاْ إِن نَّتَّبِعِ ٱلْهُدَىٰ مَعَكَ
نُتَخَطَّفْ مِنْ أَرْضِنَآ أَوَلَمْ نُمَكِّن لَّهُمْ حَرَمًا ءَامِنًا يُجْبَىٰٓ إِلَيْهِ ثَمَرَٰتُ
كُلِّ شَيْءٍ رِّزْقًا مِّن لَّدُنَّا وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿57﴾ وَكَمْ أَهْلَكْنَا
مِن قَرْيَةٍ بَطِرَتْ مَعِيشَتَهَا فَتِلْكَ مَسَٰكِنُهُمْ لَمْ تُسْكَن مِّنۢ بَعْدِهِمْ
إِلَّا قَلِيلًا وَكُنَّا نَحْنُ ٱلْوَٰرِثِينَ ﴿58﴾ وَمَا كَانَ رَبُّكَ مُهْلِكَ
ٱلْقُرَىٰ حَتَّىٰ يَبْعَثَ فِيٓ أُمِّهَا رَسُولًا يَتْلُواْ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتِنَا
وَمَا كُنَّا مُهْلِكِي ٱلْقُرَىٰٓ إِلَّا وَأَهْلُهَا ظَٰلِمُونَ ﴿59﴾

51. Haƙiƙa mun bayyana musu alƙur'ani saboda ko sa wa'azantu su bada gaskiya.

(MUMINAI DAGA AHLUL KITABI)

52. Waɗanda muka basu littafi tun gaban Alƙur'ani su masu bada gaskiya ne dashi (ta sauka cikin wadansu jama'a da suka Musulunta na Yahudu kamar Abdullahi Ibn Salamu da waninsa da wadansu kuma daga nasara sukazo daga Habasha da Sham.)
53. Idan ana karanta musu Alƙur'ani sai sukAnce "Mun bada gaskiya. haƙiƙa shi Alƙur'ani gaskiya ne daga Ubangijinmu, haƙiƙa mun kasance masu kadaita Allah tun gabansa".
54. Waɗancananka ana basu ladansu marra biyu, (saboda imani da littafi biyu da dauriyarsu bisa aiki da abinda yake cikinsu) suna ije mummunan aiki da kyakkaywan aiki suna ciyarwa daga kyakkyawan aiki, suna ciyarwa daga abinda muka arzurta musu, (wato suna sadaka da kyauta.)
55. Idan sun ji yashashshiyar magana zagi da cuta ga kafirai su sukan bijire ga barinsa (su kau da kai,) sukance ayyukanmu na garemu, naku na gareku, mun sallame ku bamu baku, mu Barna abutar masu katobara.

(RADDI KAN SASHIN RIYERIYEN MUSHURIKAI)

56. (Wannan aya ta sauka bisa kwadayin da Annabi Sallallahu alaihi wasallama yayi na musuluntar baffansa Abi Dalib). Cewa kai baka shiriyar wanda kake son (shiriyarsa,) sai dai Allah ne yake shiriyar wanda yaga dama, kuma shine masani da masu shiryuwa.
57. Mutanensa Sukace, "In mun bi shiriya taredakai a fyauce mu daga ƙasanmu" (Ubangiji yace,) "Shin bamu tabbatar musu da Harami amintacce ba ne? (Dasuke amincewa daga Hari da kisa, waɗanda suka afku daga ba'alin Larabawa bisa ba'ali) da akc kai amfanin kowane abu izuwa gareshi [1] don arzurtawa daga garemu sai dai yawaicinsu basu san (abinda muke faɗa gaskiya ne ba!)
58. Da yawa muka halakar daga mutanen alƙarya data butulce ni'imar da Allah yayi mata, wadancananka gidaddajinsune ba a zaune ta ba bayansu sai kadan (wato matafiya suna wucewa a wadancananka gurare su huta kadan su wuce). Mun tabbata mune kaɗai magadansu.
59. Ubangijinka bai kasance mai halakar da alƙaryu (doncin zali ba) saiya aiko jakada. a babban birni n tada yake karanta ayoyinmu a garesu, bamu zamo masu halakar da alkaryu ba sai face mutanen ta suna azzalumai (da ƙaryata manzanni)

1) Wannan aya ta dace da abinda na fassara aya dashi can a baya. Duba aya ta (125) a cikin BaKara wato 'Bada ciro Da'ifa daga Sham bane kadai daga duk duniya ne'Sanajiy

ثمن

وَمَا أُوتِيتُم مِّن شَيْءٖ فَمَتَاعُ الْحَيَوٰةِ الدُّنْيَا وَزِينَتُهَا وَمَا عِندَ اللَّهِ
خَيْرٌ وَأَبْقَىٰٓ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿60﴾ * أَفَمَن وَعَدْنَٰهُ وَعْدًا حَسَنًا
فَهُوَ لَٰقِيهِ كَمَن مَّتَّعْنَٰهُ مَتَاعَ الْحَيَوٰةِ الدُّنْيَا ثُمَّ هُوَ
يَوْمَ الْقِيَٰمَةِ مِنَ الْمُحْضَرِينَ ﴿61﴾ وَيَوْمَ يُنَادِيهِمْ فَيَقُولُ أَيْنَ
شُرَكَآءِيَ الَّذِينَ كُنتُمْ تَزْعُمُونَ ﴿62﴾ قَالَ الَّذِينَ حَقَّ عَلَيْهِمُ الْقَوْلُ
رَبَّنَا هَٰٓؤُلَآءِ الَّذِينَ أَغْوَيْنَا أَغْوَيْنَٰهُمْ كَمَا غَوَيْنَا تَبَرَّأْنَا إِلَيْكَ
مَا كَانُوا إِيَّانَا يَعْبُدُونَ ﴿63﴾ وَقِيلَ ادْعُوا شُرَكَآءَكُمْ فَدَعَوْهُمْ
فَلَمْ يَسْتَجِيبُوا لَهُمْ وَرَأَوُا الْعَذَابَ لَوْ أَنَّهُمْ كَانُوا يَهْتَدُونَ ﴿64﴾
وَيَوْمَ يُنَادِيهِمْ فَيَقُولُ مَاذَا أَجَبْتُمُ الْمُرْسَلِينَ ﴿65﴾ فَعَمِيَتْ
عَلَيْهِمُ الْأَنۢبَآءُ يَوْمَئِذٖ فَهُمْ لَا يَتَسَآءَلُونَ ﴿66﴾ فَأَمَّا مَن تَابَ
وَءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحًا فَعَسَىٰٓ أَن يَكُونَ مِنَ الْمُفْلِحِينَ ﴿67﴾
وَرَبُّكَ يَخْلُقُ مَا يَشَآءُ وَيَخْتَارُ مَا كَانَ لَهُمُ الْخِيَرَةُ سُبْحَٰنَ
اللَّهِ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿68﴾ وَرَبُّكَ يَعْلَمُ مَا تُكِنُّ
صُدُورُهُمْ وَمَا يُعْلِنُونَ ﴿69﴾ وَهُوَ اللَّهُ لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ
لَهُ الْحَمْدُ فِي الْأُولَىٰ وَالْآخِرَةِ وَلَهُ الْحُكْمُ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿70﴾

60. Abinda aka baku na komai, to amfanin rayuwar duniya da kyalkyalin banzar ta ne, ku more dan tsawon rayuwarku sannan ya kare, abinda yake gurin Allah (na sakamako) shine yafi amfani yafi wanzuwa, shin ba kwa hankalta (cewa mai wanzuwa shi ya.fi mai karewa ba!
61. Shin wanda mukayi masa alkawari kyakkyawa, (shi zai gamu da sakamakon alƙawarin nan aljanna,) zai zama kamar wanda muka jiyar dashi dadin rayuwar duniya (ya gushe nan ga kusa,) sannan shi a ranar alƙiyama yana daga cikin ababan shigarwa wuta. (A'a, bazasu zama ɗaya ba).

(SASHIN MATSAYIN MUSHURIKAI RANAR ALƘIYAMA)

62. Ambaci ranar da Ubangiji yake kiran su yace "Ina ababen tarayyar nawa, waɗanda kuka kasance kuna riya su (abokan tarayyagareni?)
63. Waɗanda magana ta tabbata garesu dashiga wuta, sune shiya gabannin bata, sukace ya Ubangijinmu waɗannan waɗanda muka batiir dasu mun ɓatar dasune suka bata tamfar yadda muka bata, bamu tilashe su a kan bata ba, mun kubuta daga garesu izuwa gareka basu kasance mu suke bautawa ba.
64. Akace ku kirawo gumakan naku waɗanda kuke riyawa cewa su abokan tarayya ne ga Allah, suka kira su basu amsa musu kiransu ba, suka ga azaba, dasun kasance sun shidya a duniya da basu ga azaba a Lahira ba.
65. Ka ambaci ranar da Ubangiji yake kiransu, yace me kuka amsawa manzannina izuwa gareku?
66. Sai labaru masu amfani suka makance ga barin su, a wannan rana basu samu tsira garesu a cikin su, su bazasu tamba yeyeniyar juna gareshi ba sai dai suyi shiru.
67. Amma wanda ya tubadaga shirka, ya bada gaskiya da kadaita Allah, yayi aiki na gari wato ya bada farillai, to ana kauna wannan ya kasance daga marabauta.

(JA'IZAI A HAƘƘIN ALLAH TA'ALA DA SIFOFIN KAMALA)

68. Ubangijinka yana halittar abinda yaga dama, yana zaɓin abinda yaga dama. Mushurikai basu da zaɓi a cikin komai, Tsarki ya tabbatar masa ya girma ga barin abinda suke shirkantawa(1)
69. Ubangijinka yasan abinda kirazansu take kunsa da abinda harasansu suke ɓayyanawa (na daga wancananka).
70. Shine Allah wanda babu abin bautawa da gaskiya sai shi. Godiya tana gareshi a cikin duniya da lahira, hukunci zartacce a cikin komai yana ga Allah izuwa gareshi ake komowa da ku.

1) Wannan aya tana daga? cikin ayoyin da suka nuna cewa bawa bashi da tasiri a cikin komai sai Allah, amma akwai ayoyi takwarorinta, waɗanda suke nune cewa bawa yana da tasiri a zahirin ayyukansa, wato haƙiƙa kenan da mujazi wanda malaman Tauhibi sun wadatar da maganganu a wannan matsayi don tabbatar da kasbi da tsuwur wuriko ga bawa. - Sanajiy -

قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِن جَعَلَ ٱللَّهُ عَلَيْكُمُ ٱلَّيْلَ سَرْمَدًا إِلَىٰ يَوْمِ
ٱلْقِيَٰمَةِ مَنْ إِلَٰهٌ غَيْرُ ٱللَّهِ يَأْتِيكُم بِضِيَآءٍ أَفَلَا تَسْمَعُونَ ﴿71﴾
قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِن جَعَلَ ٱللَّهُ عَلَيْكُمُ ٱلنَّهَارَ سَرْمَدًا إِلَىٰ يَوْمِ
ٱلْقِيَٰمَةِ مَنْ إِلَٰهٌ غَيْرُ ٱللَّهِ يَأْتِيكُم بِلَيْلٍ تَسْكُنُونَ فِيهِ
أَفَلَا تُبْصِرُونَ ﴿72﴾ وَمِن رَّحْمَتِهِۦ جَعَلَ لَكُمُ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ
لِتَسْكُنُوا۟ فِيهِ وَلِتَبْتَغُوا۟ مِن فَضْلِهِۦ وَلَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿73﴾
وَيَوْمَ يُنَادِيهِمْ فَيَقُولُ أَيْنَ شُرَكَآءِىَ ٱلَّذِينَ كُنتُمْ تَزْعُمُونَ ﴿74﴾
وَنَزَعْنَا مِن كُلِّ أُمَّةٍ شَهِيدًا فَقُلْنَا هَاتُوا۟ بُرْهَٰنَكُمْ
فَعَلِمُوٓا۟ أَنَّ ٱلْحَقَّ لِلَّهِ وَضَلَّ عَنْهُم مَّا كَانُوا۟ يَفْتَرُونَ ﴿75﴾
۞ إِنَّ قَٰرُونَ كَانَ مِن قَوْمِ مُوسَىٰ فَبَغَىٰ عَلَيْهِمْ وَءَاتَيْنَٰهُ
مِنَ ٱلْكُنُوزِ مَآ إِنَّ مَفَاتِحَهُۥ لَتَنُوٓأُ بِٱلْعُصْبَةِ أُو۟لِى ٱلْقُوَّةِ
إِذْ قَالَ لَهُۥ قَوْمُهُۥ لَا تَفْرَحْ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلْفَرِحِينَ ﴿76﴾
وَٱبْتَغِ فِيمَآ ءَاتَىٰكَ ٱللَّهُ ٱلدَّارَ ٱلْءَاخِرَةَ وَلَا تَنسَ نَصِيبَكَ
مِنَ ٱلدُّنْيَا وَأَحْسِن كَمَآ أَحْسَنَ ٱللَّهُ إِلَيْكَ وَلَا تَبْغِ ٱلْفَسَادَ
فِى ٱلْأَرْضِ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿77﴾

71. Cene (da mutanen Makka) "Ku bamu labari in Ubangiji yasanya muku dare tutur har izuwa ranar Alƙiyama, wane ubangiji ne ba Allah bazaizo mukuda haske (da zaku nemi abinci a cikinsa?) Shin ba kwa jin wannan (jin fahinta? Na'am).

72. Cene (dasu) "Ku bamu labari in Ubangiji yasanya rana a gareku tutur izuwa ranar Alƙiyama, wane Ubangiji ne ba Allah badazaizo mukuda dare (da zaku huta a cikinsa? Babu.) Shin ba kwa ganin (abinda kuke kai na daga kuskure ku koma ga barinsa?")

73. Yana daga jinƙan Ubangiji cewa yasanya muku dare da rana domin ku nutsu a cikinsa shi (dare) domin ku nemi falalar Ubangiji (da rana da tsuwur wuri) wata ƙila ko kwa gode masa..

74. Ka ambata ranar da yake kiransu, sai yace "Ina sharikan nawa waɗanda kuka kasance kuna riyawa?"

75. Mun fitar da shaida daga kowace al'umma (wato shine Anna-binsu da abinda suka fada) Mukace (dasu,) "Ku kawo hujjarku (a kan abinda kuka faɗa na daga shirka) suka sani, haƙiƙa cewa gaskiya (a cikin 'uluhiyya' wato sha'anin Allah) ta Allah ce kawai, (bai yi tarayya da kowa ba,) abinda suke kutawa (a cuniya na karya) ya bace musu, (shine cewa yana da shariki). Ubangiji ya girma ga barin wannan.

(ƘISSAR DUKIYA DA ILIMI DA TASIRINSU A CIKIN DUNIYAGA DAN-ADAM)

76. Haƙiƙa ƙarunu ya kasance daga mutanen Annabi Musa (Alaihissalamu) ɗan amminsa ne, (wato yas haru uban ƙaruna, Imranu mahaifin Annabi Musa 'yan uwa ne 'ya'yan Kahisa ɗan Lawi ɗan Ya'aƙuba) to sai yayi zalinci a kansu (da takabburanci da jiji dakai da yawan dukiya). Munbashi daga taskoki abin' da mabudansa lalle tana nauyayaga jama'a ma'abota karfi (Ance saba'in, Ance arba'in Ance wanin haka) yayin da mutanensa sukace dashi, "Kada kayi farin ciki da yawan dukiya (irin farin cikin girman kai) haƙiƙa Ubangiji ba yason masuyin farin ciki (da wancananka).

77. Ka nemi gidan lahira cikin abinda Allah ya baka na dukiya, kadaka mance rabonka na duniya, (wato kayi aiki a cikin ta don lahira) ka kyautata wa mutane da sadaka tamfar da Allah ya kyautata izuwa gareka, kadaka nemi ɓarna a bayan ƙasa (da aikata sabo) haƙiƙa Ubangiji ba yason maɓamata.

قَالَ إِنَّمَآ أُوتِيتُهُۥ عَلَىٰ عِلْمٍ عِندِىٓ أَوَلَمْ يَعْلَمْ أَنَّ ٱللَّهَ قَدْ أَهْلَكَ
مِن قَبْلِهِۦ مِنَ ٱلْقُرُونِ مَنْ هُوَ أَشَدُّ مِنْهُ قُوَّةً وَأَكْثَرُ جَمْعًا
وَلَا يُسْـَٔلُ عَن ذُنُوبِهِمُ ٱلْمُجْرِمُونَ ﴿78﴾ فَخَرَجَ عَلَىٰ قَوْمِهِۦ فِى زِينَتِهِۦ
قَالَ ٱلَّذِينَ يُرِيدُونَ ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَا يَٰلَيْتَ لَنَا مِثْلَ مَآ أُوتِىَ
قَٰرُونُ إِنَّهُۥ لَذُو حَظٍّ عَظِيمٍ ﴿79﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلْعِلْمَ
وَيْلَكُمْ ثَوَابُ ٱللَّهِ خَيْرٌ لِّمَنْ ءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحًا
وَلَا يُلَقَّىٰهَآ إِلَّا ٱلصَّٰبِرُونَ ﴿80﴾ فَخَسَفْنَا بِهِۦ وَبِدَارِهِ ٱلْأَرْضَ
فَمَا كَانَ لَهُۥ مِن فِئَةٍ يَنصُرُونَهُۥ مِن دُونِ ٱللَّهِ
وَمَا كَانَ مِنَ ٱلْمُنتَصِرِينَ ﴿81﴾ وَأَصْبَحَ ٱلَّذِينَ تَمَنَّوْاْ مَكَانَهُۥ
بِٱلْأَمْسِ يَقُولُونَ وَيْكَأَنَّ ٱللَّهَ يَبْسُطُ ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ
وَيَقْدِرُ لَوْلَآ أَن مَّنَّ ٱللَّهُ عَلَيْنَا لَخَسَفَ بِنَا وَيْكَأَنَّهُۥ لَا يُفْلِحُ
ٱلْكَٰفِرُونَ ﴿82﴾ * تِلْكَ ٱلدَّارُ ٱلْءَاخِرَةُ نَجْعَلُهَا لِلَّذِينَ لَا يُرِيدُونَ ثمن
عُلُوًّا فِى ٱلْأَرْضِ وَلَا فَسَادًا وَٱلْعَٰقِبَةُ لِلْمُتَّقِينَ ﴿83﴾
مَن جَآءَ بِٱلْحَسَنَةِ فَلَهُۥ خَيْرٌ مِّنْهَا وَمَن جَآءَ بِٱلسَّيِّئَةِ فَلَا يُجْزَى
ٱلَّذِينَ عَمِلُواْ ٱلسَّيِّـَٔاتِ إِلَّا مَا كَانُواْ يَعْمَلُونَ ﴿84﴾

78. Yace, ni an bani wannan dukiya ne a bisa ilimi da yake gurina, ya kasancc mafi sanin Bani-Isra'ila da Attaura bayan Annabi Musa da Annabi Haruna. Ubangiji yace, Shin bai sani bane cewa haƙiƙa Allah ya halakar da tsareku na daga gabansa wandasune mafi tsananin karfi daga gareshi, mafi yawan tarawa ga dukiya alhali yasan haka kuma Allah ya halakar dasu. Ba a tambayon masu laifi daga zunubansu, saboda saninsa da zunuban, zasu shiga wuta bada hisabi ba.

79. Sai ƙaruna yafito da mutanensa (masu yawa sun yi ado da tufofin zinare da alharini a kan dawakai da alfadarai ababan yi wa kawa.) Waɗanda suke nufin rayuwar duniya Sukace, "Wohoho, ina ma muna da misalin abinda aka ba wa ƙaruna a duniya, haƙiƙa shi ƙaruna lalle ma'abocin rabo ne mai girma.

80. Waɗanda ka basu ilimi Sukace, "kaiconku! Ladan Allah a Lahira da Aljanna shine yafi ga wanda ya bada gaskiya yayi aiki na gari (daga abinda aka ba wa ƙaruna). Ba a shigar da kowa cikin aljanna sai masu dauriya (cikin da'a, masu dauriyaga barin sabo.)

81. Sai muka kisfe ƙasa dashi da gidansa, bashi da wata jama'a da zata taimake shi ba Allah ba, (su ije masa halaka) shi bai kasance daga cikin masu taimakonsa ba.

82. Waɗanda suke burin matsayinsa a jiya suka wayi gari suna cewa, "Yi mana ki don haƙiƙa Allah Shine wanda yake yalwata arziki ga wanda yaga dama ga bayinsa, yana kuntata wa ga wanda yaga dama, ba don Allah yayi baiwa garemu ba, daya kisfe da mu. Yi mana ki da cewa haƙiƙa kafirai bazasu rabauta ba, (masu butulce ni'imar Allah kamar ƙaruna).

83. Wancananka gidan Lahira (wato Aljanna) Muna sanya ta ga waɗannan dasuke basa nufin girmama a cikin ƙasa (da basasa,) wala barna (da aikin sabo). Kyakkyawan ƙarshe ya tabbata ga masu tsoron Allah (da aiki na gari).

84. Wanda yazoda aiki na gari, to yana da fiye daga ita, (shine goma din tamkarta) wanda yazoda mummunan aiki, baza a saka wa waɗanda sukayi aiki miyagu ba sai sakamakon abinda suka kasance suna aikatawa (wato kwatankwacinsa.)

إِنَّ الَّذِي فَرَضَ عَلَيْكَ الْقُرْءَانَ لَرَآدُّكَ إِلَىٰ مَعَادٍ قُل رَّبِّي أَعْلَمُ مَن جَآءَ
بِالْهُدَىٰ وَمَنْ هُوَ فِي ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿85﴾ وَمَا كُنتَ تَرْجُوا أَن يُلْقَىٰ إِلَيْكَ
الْكِتَٰبُ إِلَّا رَحْمَةً مِّن رَّبِّكَ فَلَا تَكُونَنَّ ظَهِيرًا لِّلْكَٰفِرِينَ ﴿86﴾
وَلَا يَصُدُّنَّكَ عَنْ ءَايَٰتِ اللَّهِ بَعْدَ إِذْ أُنزِلَتْ إِلَيْكَ وَادْعُ إِلَىٰ رَبِّكَ
وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ الْمُشْرِكِينَ ﴿87﴾ وَلَا تَدْعُ مَعَ اللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ لَا إِلَٰهَ إِلَّا
هُوَ كُلُّ شَيْءٍ هَالِكٌ إِلَّا وَجْهَهُ لَهُ الْحُكْمُ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿88﴾

29 سُورَةُ العَنكَبُوتِ مَكِّيَّة
وَهِيَ تِسْعٌ وَسِتُّونَ ءَايَة 69

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ
الٓمٓ أَحَسِبَ النَّاسُ أَن يُتْرَكُوا أَن يَقُولُوا ءَامَنَّا وَهُمْ
لَا يُفْتَنُونَ ﴿1﴾ وَلَقَدْ فَتَنَّا الَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ فَلَيَعْلَمَنَّ
اللَّهُ الَّذِينَ صَدَقُوا وَلَيَعْلَمَنَّ الْكَٰذِبِينَ ﴿2﴾ أَمْ حَسِبَ الَّذِينَ
يَعْمَلُونَ السَّيِّـَٔاتِ أَن يَسْبِقُونَا سَآءَ مَا يَحْكُمُونَ ﴿3﴾ مَن كَانَ يَرْجُوا
لِقَآءَ اللَّهِ فَإِنَّ أَجَلَ اللَّهِ لَءَاتٍ وَهُوَ السَّمِيعُ الْعَلِيمُ ﴿4﴾ وَمَن
جَٰهَدَ فَإِنَّمَا يُجَٰهِدُ لِنَفْسِهِ إِنَّ اللَّهَ لَغَنِيٌّ عَنِ الْعَٰلَمِينَ ﴿5﴾

(ALBISHIR DA KOMAWAR MANZON ALLAH SALALLAHU ALAIHI WASALLAMA IZUWA MAKKA)

85. Haƙiƙa wannan daya saukar da ALƙur'ani a gareka lalle zai komar dakai izuwa Makka, alhali ya beganceta ne, Cene "Ubangijina shine masani da wanda yake cikin shiriya da wanda yazo a cikin bata mabayyani (wannan ta sauka ne don jawabi ga ƙadin kafiran Makka gareshi cewa kai kana cikin bata alhali ko shine yazo dashiriya, su sune a cikin bata).
86. Baka kasance kana ƙaunar a saukar da ƙur'ani izuwa gareka ba, sai dai an saukar dashine don jinƙai daga Ubangiji gareka, kadaka zamo mataimaki ga kafirai (a bisa addininsu wanda suka kira izuwa gareshi).

(KIRA IZUWA UBANGIJI SUBHANAHU WATA'ALA)

87. Kada kafirai su haneka ga barin ayoyin Allah bayan an saukar da ita gareka, ka kirawo (mutane) izuwa Ubangijinka, (da kaɗaita shi da bauta masa,) kadaka zamo daga cikin masu shirka (da Allah da taimakonsu).
88. Kadaka bautawa wanin Ubangiji daban tareda Allah, babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, dukkan komai halakakke ne sai zatin Allah, hukunci zartacce na ga Allah, izuwa gareshi ake komo daku (da tashi daga cikin kaburbura).

Suratul Ankabuti

A Makka Aka. Saukar Da Ita Ayoyinta Sittin Da Tara (69)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

WANNAN SURA TA ƘUNSHI HAƘIƘAR IMANI DA ABINDA YAKE SAMUN MUMINAI NA DAGA MUSIBUN ZAMANI DA ƘARFAFAR RAYUKANSU, TAREDA WANNAN, DA NASARA DA RINJAYE SUN TABBATA GA MA'ABOTA IMANI.AN ƘARFAFI WANNAN DA ƘISSOSHI DA SANYA MISALCE-MISALCE. AKWAI NATIJAR JIHADI FISABILILLAHI A CIKIN WANNAN SURA)

1.A.L.M. (Allah ne masani da wannan). Shin mutane sa zaci a barsu su dinga cewa "Mun bada gaskiya, alhali su baza a jarrabe su ba, (da abindazai bayyana haƙiƙar imanin nasu?" Wannan ta sauka ne a cikin jama'ar da suka bada gaskiya mushurikai suka cuce su).
2. Lalle mun jarrabi waɗanda suke gabansu to, lalle Allah zai nuna waɗanda suka gaskata cikin im-aninsu kowa yagansu, zakuma ya nuna maƙaryata a cikinsa.
3. Bari, wannan zato, shin waɗanda suke aikata miyagun ayyuka suna zato sa tsere mana (bazamuyi musu azaba ba? Abinda suke hukunci dashiya mugusta.
4. Duk wanda ya kasance yana tsoron saduwa da Ubangiji, to haƙiƙa ajalin saduwa da Ubangiji mai zuwa ne, to yayi tanadi da saduwar, Ubangiji mai ji ne masanine da maganganun bayi da ayyukansu.
5. Wanda yayi jihadi (na yaƙi ko ga kansa,) to shi dahir yana jihadi da kansa, (amfanin jihadin nan mai komawa ne gareshi baga Allah ba) haƙiƙa Ubangiji lalle mawadaci ne ga barin talikai (mutane da Mala'ikuda aljannu kuma mawadaci ne ga barin ibadarsu).

ربع

وَالذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ الصَّٰلِحَٰتِ لَنُكَفِّرَنَّ عَنْهُمْ سَيِّـَٔاتِهِمْ
وَلَنَجْزِيَنَّهُمْ أَحْسَنَ الذِے كَانُواْ يَعْمَلُونَ ﴿6﴾ * وَوَصَّيْنَا الْإِنسَٰنَ
بِوَٰلِدَيْهِ حُسْناً وَإِن جَٰهَدَٰكَ لِتُشْرِكَ بِے مَا لَيْسَ لَكَ بِهِۦ عِلْمٌ
فَلَا تُطِعْهُمَا إِلَيَّ مَرْجِعُكُمْ فَأُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿7﴾
وَالذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ الصَّٰلِحَٰتِ لَنُدْخِلَنَّهُمْ فِے الصَّٰلِحِينَ ﴿8﴾
وَمِنَ النَّاسِ مَنْ يَّقُولُ ءَامَنَّا بِاللَّهِ فَإِذَا أُوذِيَ فِے اللَّهِ
جَعَلَ فِتْنَةَ النَّاسِ كَعَذَابِ اللَّهِ وَلَئِن جَآءَ نَصْرٌ مِّن رَّبِّكَ
لَيَقُولُنَّ إِنَّا كُنَّا مَعَكُمُۥٓ أَوَلَيْسَ اللَّهُ بِأَعْلَمَ بِمَا فِے صُدُورِ
الْعَٰلَمِينَ ﴿9﴾ وَلَيَعْلَمَنَّ اللَّهُ الذِينَ ءَامَنُواْ وَلَيَعْلَمَنَّ
الْمُنَٰفِقِينَ ﴿10﴾ وَقَالَ الذِينَ كَفَرُواْ لِلذِينَ ءَامَنُواْ اتَّبِعُواْ سَبِيلَنَا
وَلْنَحْمِلْ خَطَٰيَٰكُمْ وَمَا هُم بِحَٰمِلِينَ مِنْ خَطَٰيَٰهُم مِّن شَےْءٍ
إِنَّهُمْ لَكَٰذِبُونَ ﴿11﴾ وَلَيَحْمِلُنَّ أَثْقَالَهُمْ وَأَثْقَالاً مَّعَ أَثْقَالِهِمْ
وَلَيُسْـَٔلُنَّ يَوْمَ الْقِيَٰمَةِ عَمَّا كَانُواْ يَفْتَرُونَ ﴿12﴾
وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا نُوحاً إِلَىٰ قَوْمِهِۦ فَلَبِثَ فِيهِمْ أَلْفَ سَنَةٍ
إِلَّا خَمْسِينَ عَاماً فَأَخَذَهُمُ الطُّوفَانُ وَهُمْ ظَٰلِمُونَ ﴿13﴾

6. Wađannan da suka bada gaskiya sukayi aiki na gargaru lalle zamu kankare miyagun ayyukansu (da ayyuka nagari,) lalle zamu saka musu da kyakkayawan abinda suka kasance suna aikatawa, (shine ayyukan nan nagargaru).

BIN IYAYE DA MATSAWAR FITINAR KAFIRAI GA MUMINAI DA FIRGITARWAR DA ALLAH YAYI WA KAFIRAI DA MUNAFUKAI)

7. Haƙiƙa munyi wa mutum wasiyya da kyautatawa ga iyayensa. In sun yaƙe ka a kan ka tara abinda baka da sani a taredani to kada kabisu, izuwa gare nine makomarku, Inbaku labari da abinda kuka kasance inbaku labari da abinda kuka kasance kuna aikatawa.
8. Wađanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru, zamu shigar dasu a cikin salihai (wato Annabawa da waliyai, wato muta shesu taredasu).
9. Akwai daga mutane wanda yake cewa "Mun bada gaskiya da Allah, idan an cuce shi (a cikin sha'anin Allah, sai yasanya cutar mutane kamar azabar Allah (a cikin tsoron azabasai yabisu yayi munafunci,) idan kuma nasara tazowa muminai daga Ubangijinka (sukayi riba,) zasu dinga cewa, ' Haƙiƙa mu mun kasance taredaku ,(a cikin imani to ku taramu a cikin ganima". Ubangiji yace,) "Shin Ubangiji bashine masani da abinda yake ƙirazan talikai ba (na imani da munafunci? Shine)
10. .Lalle Ubangiji zai nuna wađanda suka bada gaskiya (da zukatansu,) Wallahi zai nuna munafukai.
11. Wađanda suka kafirta suka fađa ga wađanda suka bada gaskiya, "Kubi addininmu ma đauke muku kusakuranku (inkun bimu", sai Ubangiji yace,) "Su bazasu đauke muku komai badaga kusakuransu, sudai maƙaryata ne (a cikin wannan").
12. Lalle zasu đauki nauyaye-nauyaye tareda nauyayensu (saboda fađinsu kubi addininmu da halakar da masu biye da addininsu,) lalle za a tambaye su ranar Alƙiyama da abinda suka kasance suna girba ƙaryaga Allah, tambaya tatursawa.

(ANNABI NUHU ALAIHISSALAMU TAREDA MUTANENSA)

13. Haƙiƙa mun aiko Annabi Nuhu (alaihissalamu) izuwa mutanensa (yana shekara arba'in (40) ko fiye) ya zauna cikinsu shekara dubu (1000) sai shekara 50 (yana kiransu izuwa Tauhidin Allah, suka ƙaryatashi) Dufanu ya kewaye dasu, suka nutse, alhali suna azzalumai (masu shirkadaAllah).

فَأَنجَيْنَٰهُ وَأَصْحَٰبَ ٱلسَّفِينَةِ وَجَعَلْنَٰهَآ ءَايَةً لِّلْعَٰلَمِينَ ﴿14﴾
ثمن * وَإِبْرَٰهِيمَ إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِ ٱعْبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱتَّقُوهُ ذَٰلِكُمْ خَيْرٌ
لَّكُمْ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿15﴾ إِنَّمَا تَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَوْثَٰنًا وَتَخْلُقُونَ
إِفْكًا إِنَّ ٱلَّذِينَ تَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ لَا يَمْلِكُونَ
لَكُمْ رِزْقًا فَٱبْتَغُواْ عِندَ ٱللَّهِ ٱلرِّزْقَ وَٱعْبُدُوهُ
وَٱشْكُرُواْ لَهُۥٓ إِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿16﴾ وَإِن تُكَذِّبُواْ فَقَدْ
كَذَّبَ أُمَمٌ مِّن قَبْلِكُمْ وَمَا عَلَى ٱلرَّسُولِ إِلَّا ٱلْبَلَٰغُ
ٱلْمُبِينُ ﴿17﴾ أَوَلَمْ يَرَوْاْ كَيْفَ يُبْدِئُ ٱللَّهُ ٱلْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥٓ
إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٌ ﴿18﴾ قُلْ سِيرُواْ فِى ٱلْأَرْضِ
فَٱنظُرُواْ كَيْفَ بَدَأَ ٱلْخَلْقَ ثُمَّ ٱللَّهُ يُنشِئُ ٱلنَّشْأَةَ
ٱلْءَاخِرَةَ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿19﴾ يُعَذِّبُ مَن يَشَآءُ
وَيَرْحَمُ مَن يَشَآءُ وَإِلَيْهِ تُقْلَبُونَ ﴿20﴾ وَمَآ أَنتُم بِمُعْجِزِينَ
فِى ٱلْأَرْضِ وَلَا فِى ٱلسَّمَآءِ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِن وَلِىٍّ
وَلَا نَصِيرٍ ﴿21﴾ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَلِقَآئِهِۦٓ أُوْلَٰٓئِكَ
يَئِسُواْ مِن رَّحْمَتِى وَأُوْلَٰٓئِكَ لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿22﴾

14. Muka tserar da Annabi Nuhu (Alaihissalamu) da ma'abota jirgi (wađanda suka kasance taredashi a cikinta,) muka sanya ta izna ga talikai dasuke bayansu in sun sabi manzanninsu, Annabi Nuhu ya rayu bayan đufana shekara sittin (60) ko fiye har mutane sukayi yawa).

(ƘISSAR ANNABI IBRAHIM ALAIHISSALAMU DA MUTANENSA)

15. Ka ambaci Annabi Ibrahim (alaihissalamu) lokacin daya fađa ga mutanensa, ku bautawa Allah kuji tsoron Sa, wancananku shi yafi amfani gareku (daga abinda kuke kai na bautar gumaka,) inkun kasance kun san (alheri daga waninsa to ku aikata abinda aka fađa muku).
16. Dahir kuna bautawa wanin Allah, gumaka kuna girba ƙarya, haƙiƙa wađanda kuke bautawa ba Allah ba, basu mallaki arziki gareku ba, (bazasu iya azurta ku ba,) to ku nemi arziki nan ga Allah, ku bauta masa, ku gode masa, izuwa gareshi ake komawa daku.
17. Inkun ƙaryata ni (yaku mutanen Makka) to haƙiƙa an ƙaryata al'ummomi nadaga gabanku, ba wani abu bisa manzo illa isar da aike iyarwa mabayyani, (wannan rarraShine bisa manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama a cikin ƙissar guda biyu).
18. (Ubangiji ya fađa,) "Shin basuyi duba bane yaye Allah yake farar halitta, sannan ya mayar da halittar tamfar daya faresu, haƙiƙa wancananka abin (ambato nadaga halitta ta farko data biyu,) mai sauƙine bisa Ubangiji (yaya suke musun na biyun).
19. Cene (dasu) "Kuyi tafiya a cikin ƙasa ku duba yaya Allah ya fara halitta (ga wanda ya kasance gabanku, ya matar dasu sannan Ubaugiji ya fari tashi na ƙarshe Haƙiƙa Ubangiji mai ikone bisa komai, (yana daga gareshi farawa da komowa).
20. Yana azaba ga wanda yaga dama, yana jinƙan wanda yaga dama, izuwa gareshi ake mayar daku.
21. Ku baku zamo masu gajiyar da Ubangijinku (ga barin riskarku) a cikin ƙasa) wala a cikin sama, (da kun kasance a cikinta bazaku tserewa Allah ba) bakuda wani majiɓinci (dazai hana muku azabar Ubangiji) ba Allah ba, wala mai taimako (dazai taimake ku gaburan azabar Ubangiji.
22. Wađannan da suka kafirce da ayoyin Allah Alƙur'ani da saduwa dashi (tashin alƙiyama,) wađancananka sun debe haso daga rahamata (ai aljannata) wađancananka azabata tabbata garesu.

فَمَا كَانَ جَوَابَ قَوْمِهِۦٓ إِلَّآ أَن قَالُواْ ٱقْتُلُوهُ أَوْ حَرِّقُوهُ
فَأَنجَىٰهُ ٱللَّهُ مِنَ ٱلنَّارِ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوْمٖ
يُؤْمِنُونَ ﴿23﴾ وَقَالَ إِنَّمَا ٱتَّخَذْتُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ أَوْثَٰنٗا مَّوَدَّةَ
بَيْنِكُمْ فِي ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ثُمَّ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ يَكْفُرُ بَعْضُكُم
بِبَعْضٖ وَيَلْعَنُ بَعْضُكُم بَعْضٗا وَمَأْوَىٰكُمُ ٱلنَّارُ
وَمَا لَكُم مِّن نَّٰصِرِينَ ﴿24﴾ ۞ فَـَٔامَنَ لَهُۥ لُوطٞ
وَقَالَ إِنِّي مُهَاجِرٌ إِلَىٰ رَبِّيٓ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿25﴾
وَوَهَبْنَا لَهُۥٓ إِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ وَجَعَلْنَا فِي ذُرِّيَّتِهِ
ٱلنُّبُوٓءَةَ وَٱلْكِتَٰبَ وَءَاتَيْنَٰهُ أَجْرَهُۥ فِي ٱلدُّنْيَا وَإِنَّهُۥ
فِي ٱلْأٓخِرَةِ لَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿26﴾ وَلُوطًا إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِۦٓ
إِنَّكُمْ لَتَأْتُونَ ٱلْفَٰحِشَةَ مَا سَبَقَكُم بِهَا مِنْ أَحَدٖ
مِّنَ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿27﴾ أَئِنَّكُمْ لَتَأْتُونَ ٱلرِّجَالَ وَتَقْطَعُونَ ٱلسَّبِيلَ ﴿28﴾
وَتَأْتُونَ فِي نَادِيكُمُ ٱلْمُنكَرَ فَمَا كَانَ جَوَابَ
قَوْمِهِۦٓ إِلَّآ أَن قَالُواْ ٱئْتِنَا بِعَذَابِ ٱللَّهِ إِن كُنتَ مِنَ
ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿29﴾ قَالَ رَبِّ ٱنصُرْنِي عَلَى ٱلْقَوْمِ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿30﴾

ربع

23. (Ubangiji Subhanahu wata'ala ya faɗa a cikin ƙissar Annabi Ibrahim alaihissalam) ba abinda ya zan.a jawabin mutanensa sai cewarsu ku kashe shi koku ƙone shi, sai Ubangiji ya tserar dashi daga wuta (wacce suka jefa shi a cikinta, shine yasanya mata sanyi da aminci,) haƙiƙa a cikin wancananka (tserarwa) akwai ayoyi (shine rashin tasirin ta (wutar) a cikinsa tareda girmantada bicewar ta, da samar da dausayi maimakon ta a lokaci kaɗan) ga mutane masu gasgatawa (da kadaita Allah da ikonsa, domin sune masu amfani da ita").
24. (Annabi Ibrahim yace,) "Dahir kun riƙi gumaka (da kuke bauta mata) ba Allah ba don soyayya da take tsakaninku a cikin rayuwar duniya, sannan ranar Alƙiyama sashinku zai kafirce ga sashi, (shiwagabanni zasu kubuta daga mabiyarsu) ba'alinku zai tsine wa ba'ali, (wato mabiya zasu tsine wa shiwagabanni jahannama ce makomar ku baki ɗaya, bakuda masu hana muku azabar Ubangiji.
25. Sai Annabi Luɗu yabada gaskiya da Annabi Ibrahimu, (shi ɗan ɗan uwnsa ne Haranu), Annabi Ibrahim yace, "Ni mai ƙaura ne) izuwa Ubangijina, (wato inda Ubangijina ya umarce ni, wato yayi hijira daga Iraƙi zuwa Sham, ya sauka Khirrana shi da matarsa, Luɗu danɗan uwansa yana ɗan shekara ishirin da biyar (25). Sai Annabi Ibrahim alaihissalamu yace,) "Ubangiji shine mabuwayi (a cikin mulkinsa) gwani (a cikin aikinsa).
26. Muka bashi Ishaƙa bayan Isma'ila, muka bashi Ya'aƙuba bayan Ishaƙa, muka sanya Annabci cikin zuriyarsa da duk Annabawa bayan Annabi Ibrahim daga zuriyarsa suke da littattafai-Attaura, Injila da Zabura da Furƙani, Mun bashi ladansa a duniya shine yabo kyakkyawa a cikin addini, haƙiƙa shi a cikin Lahira yana cikin salihai.

(ƘISSAR ANNABI LUƊU ALAIHISSALAMU TAREDA MUTANENSA)

27. Ambaci Annabi Luɗu (alaihissalamu,) zamanin daya faɗa ga mutanensa yanzu haƙiƙa ku mutanena kwa dinga zuwa da aikin alfasha (shine buƙatar mazaje wacce wani daga talikai bai ngaye kuda ita ba mutum ko aljan?
28. Yanzu kwa dinga zuwa mazaje kuna yanke hanya ta masu wucewa da aikin ɓarna da wanda yake wucewa daku, sai mutane suka bar wucewa ta gurin.
29. Kuna aikata aikin munkari a gurin zamanku aikin alfasha ba'alinku ga ba'ali, wato a indasuke zaune. Jawabin mutanensa bai kasance basai sukace kazo mana da azabar Allah inka kasance daga masu gaskiya a cikin wannan.
30. Sai yace Ubangiji ka taimake ni a cikin sa a kan mutane maɓarnata sai Allah ya amsa masa addu'arsa.

وَلَمَّا جَآءَتْ رُسُلُنَآ إِبْرَٰهِيمَ بِالْبُشْرَىٰ قَالُوٓاْ إِنَّا
مُهْلِكُوٓاْ أَهْلِ هَٰذِهِ الْقَرْيَةِ إِنَّ أَهْلَهَا كَانُواْ ظَٰلِمِينَ ﴿31﴾
قَالَ إِنَّ فِيهَا لُوطاً قَالُواْ نَحْنُ أَعْلَمُ بِمَن فِيهَا
لَنُنَجِّيَنَّهُۥ وَأَهْلَهُۥٓ إِلَّا امْرَأَتَهُۥ كَانَتْ مِنَ الْغَٰبِرِينَ ﴿32﴾
وَلَمَّآ أَن جَآءَتْ رُسُلُنَا لُوطاً سِيٓءَ بِهِمْ وَضَاقَ بِهِمْ
ذَرْعاً وَقَالُواْ لَا تَخَفْ وَلَا تَحْزَنْ إِنَّا مُنَجُّوكَ وَأَهْلَكَ
إِلَّا امْرَأَتَكَ كَانَتْ مِنَ الْغَٰبِرِينَ ﴿33﴾ إِنَّا مُنزِلُونَ
عَلَىٰٓ أَهْلِ هَٰذِهِ الْقَرْيَةِ رِجْزاً مِّنَ السَّمَآءِ بِمَا كَانُواْ
يَفْسُقُونَ ﴿34﴾ وَلَقَد تَّرَكْنَا مِنْهَآ ءَايَةَۢ بَيِّنَةً لِّقَوْمٍ
يَعْقِلُونَ ﴿35﴾ * وَإِلَىٰ مَدْيَنَ أَخَاهُمْ شُعَيْباً فَقَالَ يَٰقَوْمِ ثمن
اعْبُدُواْ اللَّهَ وَارْجُواْ الْيَوْمَ ءَالَاخِرَ وَلَا تَعْثَوْاْ فِي الْأَرْضِ
مُفْسِدِينَ ﴿36﴾ فَكَذَّبُوهُ فَأَخَذَتْهُمُ الرَّجْفَةُ
فَأَصْبَحُواْ فِي دَارِهِمْ جَٰثِمِينَ ﴿37﴾ وَعَاداً وَثَمُوداً
وَقَد تَّبَيَّنَ لَكُم مِّن مَّسَٰكِنِهِمْ وَزَيَّنَ لَهُمُ الشَّيْطَٰنُ
أَعْمَٰلَهُمْ فَصَدَّهُمْ عَنِ السَّبِيلِ وَكَانُواْ مُسْتَبْصِرِينَ ﴿38﴾

31. Yayin da jakadanmu manzanninmu suka zowa Ibrahimu da. albishir, sai sukace haƙiƙa mu zamu halakar da wannan alƙarya, to Annabi Luđu saboda mutaneta sun kasance kafirai, wato wađannan aiyuka sun ƙunsu cikin kafircin ne.
32. Annabi Ibrahimu yace akwai Annabi Luđu a cikinta, sai sukace; mune masana da wanda yake cikinta, lalle zamu tserar dashi da mutanensa sai matarsa, wannan ta kasance cikin masu wanzuwa cikin azaba.
33. Yayin da manzanninmu suka zowa Annabi Luđu alaihissalamu sai yayi baƙin ciki dasu, ƙirjinsa ya ƙuntata saboda su , don masu kyan maganane a surar baƙi, sai yaji tsoron mutanensa a kansu sai sukace mu jakadun Ubangijinka ne, sukace kada kaji tsoro kada kayi baƙin ciki, haƙiƙa mu masu tserar dakai ne da lyalinka sai matarka ta kasance daga masu wanzuwa cikin azaba.
34. Haƙiƙa mu masu saukar da azabane bisa mutanen wannan gari daga sama saboda kasancewarsu fasiƙai.
35. Haƙiƙa mun bar aya daga garetashine guraban kangonta ga mutane masu hankali.

(ƘISSAR MUDYANU DA ADU DA SAMUDU DA WANINSU)

36. Mun aiko Annabi Shu'aibu alai-hissalamu izuwa Madyana đan uwansu, yace "Yaku mutanena ku bautawa Allah ku ƙaunaci ranar Lahira, kada kuyi ɓarna a bayan ƙasa kuna masuyin ta'adi.
37. Suka ƙaryatashi sai girgizata danke su suka wayi gari a durkushe a kan gwiwoyinsu a cikin gidaddajinsu, suna mace.
38. Mun halakar da Adu da Samudu, haƙiƙa halakarwar da mukayi musu ta bayyana gareku, daga mazaunansu a Hijiru dayaman. Shaiđan ya ƙawata musu ayyukansu na kafirci da saɓon Allah, ya taresu ga barin hanyar gaskiya, sun kasance ma'abota basira.

وَقَٰرُونَ وَفِرْعَوْنَ وَهَٰمَٰنَ ۖ وَلَقَدْ جَآءَهُم مُّوسَىٰ
بِٱلْبَيِّنَٰتِ فَٱسْتَكْبَرُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ وَمَا كَانُوا۟ سَٰبِقِينَ ﴿39﴾
فَكُلًّا أَخَذْنَا بِذَنۢبِهِۦ ۖ فَمِنْهُم مَّنْ أَرْسَلْنَا عَلَيْهِ حَاصِبًا
وَمِنْهُم مَّنْ أَخَذَتْهُ ٱلصَّيْحَةُ وَمِنْهُم مَّنْ خَسَفْنَا بِهِ ٱلْأَرْضَ
وَمِنْهُم مَّنْ أَغْرَقْنَا ۚ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيَظْلِمَهُمْ وَلَٰكِن
كَانُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ يَظْلِمُونَ ﴿40﴾ مَثَلُ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُوا۟
مِن دُونِ ٱللَّهِ أَوْلِيَآءَ كَمَثَلِ ٱلْعَنكَبُوتِ ٱتَّخَذَتْ بَيْتًا ۖ
وَإِنَّ أَوْهَنَ ٱلْبُيُوتِ لَبَيْتُ ٱلْعَنكَبُوتِ ۖ لَوْ كَانُوا۟
يَعْلَمُونَ ﴿41﴾ إِنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا يَدْعُونَ مِن دُونِهِۦ
مِن شَىْءٍ ۚ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿42﴾ وَتِلْكَ ٱلْأَمْثَٰلُ
نَضْرِبُهَا لِلنَّاسِ ۖ وَمَا يَعْقِلُهَآ إِلَّا ٱلْعَٰلِمُونَ ﴿43﴾
خَلَقَ ٱللَّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ بِٱلْحَقِّ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ
لَءَايَةً لِّلْمُؤْمِنِينَ ﴿44﴾ ٱتْلُ مَآ أُوحِىَ إِلَيْكَ مِنَ ٱلْكِتَٰبِ
وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ ۖ إِنَّ ٱلصَّلَوٰةَ تَنْهَىٰ عَنِ ٱلْفَحْشَآءِ وَٱلْمُنكَرِ ۗ
وَلَذِكْرُ ٱللَّهِ أَكْبَرُ ۗ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ مَا تَصْنَعُونَ ﴿45﴾

39. Haƙiƙa mun halakar da ƙarunu da Fir'auna da Hamanu, haƙiƙa Annabi Musa yazo musu da hujjoji mabayyana sukayi girmankai a cikin ƙasa, basu kasance masu tserewa azabarmu ba.
40. To kowanne daga mutanen mun kamasu ɗaiɗai, akwai daga cikinsu wanda muka aiko iska mai jifa da tsakwankwani a ga-reshi kamar mutanen Annabi Luđu, akwai daga garesu wanda tsawa ta kamashi kamar Samudu, akwai daga garesu wanda muka kisfe ƙasa dashi kamar ƙaruna, akwai daga garesu wanda muka nutsar dashi kamar mutanen Annabi Nuhu da Fir'auna da mutanensa. Ubangiji bai tabbata mazalinci a garesu ba, yayi musu azaba bada zunubi ba, saidai sun kasance kansu suke zalintada aikata zunubi.
41. Misalin waɗanda suka riƙi wanin Allah iyayen giji wato gumaka, saboda ƙaunar amfanin ta kamar gizo-gizo ce data riƙi ɗaki ga kanta, da take taruwa izuwa gareshi, haƙiƙa mafi raunin ɗakuna lalle ɗakin gizo-gizo baya maganin zafi baya maganin sanyi, dasun kasance sunsan haka da basu bauta musu ba.
42. Haƙiƙa Ubangiji yasan abinda suke bautawa ba Allah ba nako mene ne, Ubangiji mabuwayi ne cikin mulkinsa, gwanine cikin aikinsa.
43. Waɗancananka misalce-misalce a cikin Alƙur'ani muna sanyata ne a cikin mutane amma babu mai fahintarta sai masu lura.
44. Ubangiji ya halicci sammai da ƙassaida gaskiya, haƙiƙa akwai aya a cikin wancananka mai shiryarwa ga muminai.

(LADABCE-LADABCE NA MUSULUNCI WATO KULAWA DA SALLAH DA YAWAITAWA GA AMBATON ALLAH)

45. Karanta abinda aka aiko izuwa gareka na Alƙur'ani ka inganta tsaiwar sallah, haƙiƙa sallah tana hana aikin alfasha da aikin munkari muddar mutum yana cikin aikinta, lalle ambaton Allah shine mafi girma daga waninsa na daga ɗa'o'i. Allah yasan abinda kuke aikatawa na hairi ko sharri, zaiyi muku sakamako dashi.

حزب

۞ وَلَا تُجَٰدِلُوٓاْ أَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ إِلَّا بِٱلَّتِي هِيَ أَحۡسَنُ إِلَّا ٱلَّذِينَ
ظَلَمُواْ مِنۡهُمۡۖ وَقُولُوٓاْ ءَامَنَّا بِٱلَّذِيٓ أُنزِلَ إِلَيۡنَا وَأُنزِلَ إِلَيۡكُمۡ
وَإِلَٰهُنَا وَإِلَٰهُكُمۡ وَٰحِدٞ وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ ﴿46﴾ وَكَذَٰلِكَ
أَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَۚ فَٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ يُؤۡمِنُونَ بِهِۦۖ
وَمِنۡ هَٰٓؤُلَآءِ مَن يُؤۡمِنُ بِهِۦۚ وَمَا يَجۡحَدُ بِـَٔايَٰتِنَآ
إِلَّا ٱلۡكَٰفِرُونَ ﴿47﴾ وَمَا كُنتَ تَتۡلُواْ مِن قَبۡلِهِۦ مِن كِتَٰبٖ
وَلَا تَخُطُّهُۥ بِيَمِينِكَۖ إِذٗا لَّٱرۡتَابَ ٱلۡمُبۡطِلُونَ ﴿48﴾ بَلۡ هُوَ ءَايَٰتُۢ
بَيِّنَٰتٞ فِي صُدُورِ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَۚ وَمَا يَجۡحَدُ بِـَٔايَٰتِنَآ
إِلَّا ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿49﴾ وَقَالُواْ لَوۡلَآ أُنزِلَ عَلَيۡهِ ءَايَٰتٞ مِّن رَّبِّهِۦۖ
قُلۡ إِنَّمَا ٱلۡأٓيَٰتُ عِندَ ٱللَّهِ وَإِنَّمَآ أَنَا۠ نَذِيرٞ مُّبِينٌ ﴿50﴾
أَوَلَمۡ يَكۡفِهِمۡ أَنَّآ أَنزَلۡنَا عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ يُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡۚ
إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَرَحۡمَةٗ وَذِكۡرَىٰ لِقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ﴿51﴾
قُلۡ كَفَىٰ بِٱللَّهِ بَيۡنِي وَبَيۡنَكُمۡ شَهِيدٗاۖ
يَعۡلَمُ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۗ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
بِٱلۡبَٰطِلِ وَكَفَرُواْ بِٱللَّهِ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ﴿52﴾

(YADDA AKE KIRAN AHLUL-KITABI IZUWA MUSULUNCI)

46. Kada kuyi jayayya da mazowa littafi sai jayayya wacce take mafi kyau (wato ma'ana kada kuyi kira izuwa addinin Allah saida taushi da laushi bada kaushi ba, kamar kira izuwa Allah da ayoyinsa da fadakarwa a kan hujjojinsa) sai wadanda sukayi zalunci daga cikinsu, sai wadanda suka hanu ga abinda aka hanesu shine suka yakeku ko sukaki bada jiziya, to ku yakesu da kansakali harsu Musulunta kosu bada jiziyaku fadawa mutane wadanda sukayi furuci da jiziyar nan, in sun baku labari da wani abu da yake cikin littafinsu mun bada gaskiya da abinda aka saukar izuwa garemu da abinda ka saukar izuwa gareku, ma'ana kadaku ,karyata su, kadaku ,gasgatasu a cikin wancananka, Ubangijinmu da ubangijinku dayane, mu masu mika wuya ne gareshi.

47. Tamfar yadda muka saukar da Attaura garesu hakana muka saukar maka da Alkr'ani, wadanda muka basu Attaura (kamar Abdullahi bin Salami da waninsa) sun bada gaskiya da Alkur'ani, akwai daga wadannan mutane na Makka wanda yabada gaskiya dashi, barnai musu da ayoyinmu (bayan bayyanar ta) sai kafirai (wato Yahudu sun sani sarai cewa Alkur'ani gaskiya ne wanda yazo dashi mai gaskiya ne sukayi musun wancananka).

48. Baka kasance kana karantawar littafi gaban Alkur'ani ba wala ka rubutashi da hannunka, daka kasance mai karatu mai rubutu, da mabarnata (sunc Yahudawa) dasunyi kokonto (a cikinka, dasunce wanda yake cikin Attaura baya karatu baya rubutu).

49. Bari, shi Alkur'ani (wanda kazo dashi) ayoyi ne mabayyana a cikin zukatan wadanda aka basu ilimi (wato muminai su haddace shi,) barnai musu da ayoyinmu sai azzalumai (wato Yahudawa, sunyi musunta bayan bayyanar ta garesu.

(AMBATON WADANSU RIKICE-RIKICEN DA MAYAR DA AMSA A KANSU)

50. Kafiran Makka sukace "Donme ba a saukar da ayoyi ga Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) daga Ubangijinsa (kamar taguwar Annabi Salihu da sandar Annabi Musa da kabakin Annabi Isa,) cene (dasu) "Dahir, ayoyi daga Allah suke, yana saukar da ita yadda yaga dama, nidai mai gargadi ne (da wuta ga mazowa sabo,) mabayyanin gargadi ".

51. Shin bai ishesu bane (cikin abinda suka nema) cewa mun saukar da Alkur'ani gareka da ake karantashi garesu (to shi ayane a garesu mai zarcewa ba tukewa gareta sabanin abinda aka ambata na daga ayoyi. Hakika akwai rahama a cikin wancananka (littafi) da gargadi ga mutane masu bada gaskiya (da Allah).

52. Cene "Ubangiji Allah 'ya isa shaida tsakanina daku, yasan abinda yake sammai da kassai, (halina da halinku yana daga cikin sanin Ubangiji), wadanda suka bada gaskiya da karya (shine abinda ake bautawa ba Allah ba) suka kafirtada Allah (daga cikinku,) wadancananka sune hakikanin tababbu (a cikin kudurin cinikinsu saboda sun sayi kafirci da imani).

وَيَسْتَعْجِلُونَكَ بِالْعَذَابِ وَلَوْلَا أَجَلٌ مُّسَمًّى لَّجَآءَهُمُ الْعَذَابُ
وَلَيَأْتِيَنَّهُم بَغْتَةً وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿53﴾ يَسْتَعْجِلُونَكَ بِالْعَذَابِ
وَإِنَّ جَهَنَّمَ لَمُحِيطَةٌ بِالْكَافِرِينَ ﴿54﴾ يَوْمَ يَغْشَاهُمُ الْعَذَابُ
مِن فَوْقِهِمْ وَمِن تَحْتِ أَرْجُلِهِمْ وَيَقُولُ ذُوقُواْ مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿55﴾
يَا عِبَادِيَ الَّذِينَ ءَامَنُواْ إِنَّ أَرْضِي وَاسِعَةٌ فَإِيَّايَ فَاعْبُدُونِ ﴿56﴾
كُلُّ نَفْسٍ ذَآئِقَةُ الْمَوْتِ ثُمَّ إِلَيْنَا تُرْجَعُونَ ﴿57﴾ وَالَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ الصَّالِحَاتِ لَنُبَوِّئَنَّهُم مِّنَ الْجَنَّةِ غُرَفًا تَجْرِي مِن تَحْتِهَا
الْأَنْهَارُ خَالِدِينَ فِيهَا نِعْمَ أَجْرُ الْعَامِلِينَ ﴿58﴾ الَّذِينَ صَبَرُواْ وَعَلَىٰ
رَبِّهِمْ يَتَوَكَّلُونَ ﴿59﴾ * وَكَأَيِّن مِّن دَآبَّةٍ لَّا تَحْمِلُ رِزْقَهَا ثمن
اللَّهُ يَرْزُقُهَا وَإِيَّاكُمْ وَهُوَ السَّمِيعُ الْعَلِيمُ ﴿60﴾ وَلَئِن سَأَلْتَهُم
مَّنْ خَلَقَ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضَ وَسَخَّرَ الشَّمْسَ وَالْقَمَرَ لَيَقُولُنَّ اللَّهُ
فَأَنَّىٰ يُؤْفَكُونَ ﴿61﴾ اللَّهُ يَبْسُطُ الرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ مِنْ
عِبَادِهِ وَيَقْدِرُ لَهُ إِنَّ اللَّهَ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمٌ ﴿62﴾ وَلَئِن سَأَلْتَهُم
مَّن نَّزَّلَ مِنَ السَّمَآءِ مَآءً فَأَحْيَا بِهِ الْأَرْضَ مِن بَعْدِ مَوْتِهَا
لَيَقُولُنَّ اللَّهُ قُلِ الْحَمْدُ لِلَّهِ بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْقِلُونَ ﴿63﴾

53. Suna neman gaggawarka da azaba, badon ajali abin ambato (da azaba ba) da azabar tazo musu (a gaggauce,) Wallahi lalle azabar nan zatazo musu barabe, (wato afujajan) alhali basu san lokacin zuwanta ba.)
54. Suna neman gaggawarka da azaba a duniya, haƙiƙa jahannama mai kewayewa ce da kafirai.
55. Ranar da azaba take lullube su daga burbushinsu kuma daga ƙarƙashin ƙafafuwansu (Shi mala'ikan da aka wakkala dayi musu azaba) zaice, ku ɗanɗani abinda kuka kasance kuna aikatawa, (wato sakamakonsa, bazaku tsere manaba!)

(NASIHOHI NA UBANGIJI IZUWA MUSULMI DA WAJABCIN HIJIRA DAGA ƘASA IZUWA ƘASA)

56. Yaku bayina waɗanda suka bada gaskiya, haƙiƙa ƙasata mayalwaciyace, toni kaɗai saiku bauta min, (wato ku bauta mini ni kaɗai a kowace ƙasa ibadata sauwaƙa a ciki, shine kuyi hijira izuwa gareta wato ƙaura izuwa gareta daga ƙasar da ibada bata sauwaƙa a cikiba. Ta sauka a cikin raunanan Musulmin Makka sun kasance a cikin ƙunci na daga bayyana Musulunci a cikinta.) [1]

(WA'AZI DA MUTUWA GA DUKKAN MUSULMI)

57. Dukkan rai zata ɗanɗani mutuwane, sannan izuwa garemu za a komo daku.
58. waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki na gargaru zamu saukar dasu a cikin aljanna a benaye, ƙoramu suna kwarara ƙarƙashinta masu dauwama a cikinta, madalla ladan masu aiki (wannan lada).
59. Sune waɗanda suka daure (a kan cutar mushurikai da hijira saboda bayyana addini,) kuma suke dogaro bisa Ubangijinsu (shi kaɗai ya azurtasu ta inda basa zato).
60. Da yawa daga dabbada bata ɗaukan arzikinta (saboda rauninta,) Allah ne mai azurtata daku (yaku waɗannan muhajirai koda ba guzuri bakuɗi a taredaku,) Allah shine maiji mai gani (da maganganunkuda zuciyoyinku).[2]
61. Wallahi inka tambayi kafirai waya halicci sammai da ƙassai, waya hore rana da wata? Zasu ce dakai Allah ne, to yaya ake juyar daku (ga barin kaɗaita Allah bayan tabbatarwarku dashi).
62. Allah ne mai yalwata arziki ga wanda yaga dama (don gwadawa,) shine kuma mai ƙuntatawa ga wanda yaga dama (bayan yalwatawa don gwadawa). Haƙiƙa Ubangiji masanine (da komai). yasan gurin dazai yalwata, yasan gurin dazai kuntata, wato wanda ya yalwa-tawa da wandazai kuntatawa).
63. Wallahi inka tambaye su waye ya saukar da ruwa daga sama ya raya ƙasa dashi bayan ƙeƙashewarta, Wallahi zasu ce dakai "Allah ne". (To yaya suke shirkantawa dashi,) cene (dasu) "Godiya ta tabbata ga Allah (bisa tabbatar hujja a kanku)" bari, yawaicinsu basa hankaltar (hauragiyarsu).

1) Farkon wanda yabi wannan umarni na wannan aya shine Sayyidina Rasulullahi Sallallahu alaihi wasallama, daya ƙaura daga Makka izuwa Madina, kuma har Musulmi sukayi kwaikwayo dashi kamar Shehu Usman ɗan Fodiyo Allah ya kara masa yarda. Hijira tana kan dukkan Mu-sulmi har alƙiyama. A duba littafin "Baya-nu wujubil Hijirati" na Shehu Usman Allah ya kara masa yarda - Sanajiy -
2) Wannan aya bata hana riƙo da musababiy ba, wanda yayi musun musabbabiy, to ya halaka, aduba (SAWI)

وَمَا هَٰذِهِ ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَا إِلَّا لَهْوٌ وَلَعِبٌ وَإِنَّ ٱلدَّارَ ٱلْءَاخِرَةَ
لَهِيَ ٱلْحَيَوَانُ لَوْ كَانُوا۟ يَعْلَمُونَ ﴿64﴾ فَإِذَا رَكِبُوا۟ فِي ٱلْفُلْكِ دَعَوُا۟
ٱللَّهَ مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ فَلَمَّا نَجَّىٰهُمْ إِلَى ٱلْبَرِّ إِذَا هُمْ يُشْرِكُونَ ﴿65﴾
لِيَكْفُرُوا۟ بِمَا ءَاتَيْنَٰهُمْ وَلِيَتَمَتَّعُوا۟ فَسَوْفَ يَعْلَمُونَ ﴿66﴾ أَوَلَمْ يَرَوْا۟
أَنَّا جَعَلْنَا حَرَمًا ءَامِنًا وَيُتَخَطَّفُ ٱلنَّاسُ مِنْ حَوْلِهِمْ أَفَبِٱلْبَٰطِلِ يُؤْمِنُونَ
وَبِنِعْمَةِ ٱللَّهِ يَكْفُرُونَ ﴿67﴾ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا
أَوْ كَذَّبَ بِٱلْحَقِّ لَمَّا جَآءَهُۥٓ أَلَيْسَ فِي جَهَنَّمَ مَثْوًى لِّلْكَٰفِرِينَ ﴿68﴾
وَٱلَّذِينَ جَٰهَدُوا۟ فِينَا لَنَهْدِيَنَّهُمْ سُبُلَنَا وَإِنَّ ٱللَّهَ لَمَعَ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿69﴾

30 سُورَةُ الرُّومِ مَكِّيَّةٌ
وَهِيَ سِتُّونَ ءَايَةً 60

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓمٓ غُلِبَتِ ٱلرُّومُ ﴿1﴾ فِيٓ أَدْنَى ٱلْأَرْضِ وَهُم مِّنۢ بَعْدِ
غَلَبِهِمْ سَيَغْلِبُونَ ﴿2﴾ فِي بِضْعِ سِنِينَ لِلَّهِ ٱلْأَمْرُ مِن قَبْلُ
وَمِنۢ بَعْدُ وَيَوْمَئِذٍ يَفْرَحُ ٱلْمُؤْمِنُونَ ﴿3﴾ بِنَصْرِ ٱللَّهِ
يَنصُرُ مَن يَشَآءُ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿4﴾

64. Wannan rayuwar duniya bata kasance basai shagala da abinda bashi da amfani da wasa, haƙiƙa gidan Lahira Itace rayuwa dauwamammiya, dasunsan haka da basu fifita duniya a kanta ba.

(WASU DAGA CIKIN MIYAGUN HALAYEN KAFIRAI)

65. Idan suka shiga cikin jirgi sai sukan roƙi Ubangiji suna masu tsarkakewar addu'a a gareshi (basa tara kowa taredashi a cikin addu'a saboda kasancewarsu cikin tsanani wanda barnai yaye musu sai Allah) a yayın daya tserar dasu izuwa gaci sai gashi suna shirkantawa da Ubangiji.

66. Donsu kafirce abinda muka basu (na daga ni'ima saboda kuma suji daɗi (da tattararsu a kan bautar gumaka,) da sannu saga aƙibar lamarinsu.

67. Shin basu saniba cewa mu mun sanyagarinsu Makka; Harami amintacce da hurumi amintacce ana ƙyauce mutane daga daura dasu (kisa da ribacewa amma bandasu?) Shin da banzasuke bada gaskiya (wato gunki) kuma suke kafirce wa ni'imar Ubangiji (saboda shirkantawa dashi?)

68. Babu mafi zalinci daga wanda ya ƙagi ƙarya bisa Allah koya ƙaryatada manzon Allah sallallahu alaihi wasallama ko Alƙur'ani yayin dayazo masa. Shin matabbacin kafirai ba cikin jahannama yake bane? (A ciki yake).

(SHAIDA DAGA UBANGIJI DA CEWA DARIKUN SUFAYE DUKKANSU NA ALLAH NE, KUMA DUKKANSU MASU SADAWA NE IZUWA UBANGIJI HAR ABADA, KUMA DA SHAI-DA A KAN SUFAYE DA CEWASU SUNA TAREDA ALLAH DON SUN ,E MASU MUƘAMIN IHSANI DA FALALAR MUJAHADA, WATO YAƘAR ZUCIYA)

69. Waɗannan da suka yaƙi son zuciyarsu a cikin neman yardarmu, lalle zamu shiryar dasu tafarku masu shiryarwa izuwa garemu, haƙiƙa Allah yana tareda masanansa a matsayin ihsani (wato sune Sufaye, Allah ya ƙara yarda a garesu, amin a duba (Sawi) da maganganun malaman haƙiƙa).

Suratur Rumi

A Makka Aka. Saukar Da Ita Ayoyinta Hamsin Da Tara (59)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

(WANNAN SURA TA TABBATAR DA BA'ALIN SIFOFIN ALLAH WAJIBABBU GARESHI, DA BAYANIN CEWA MUSULUNCI ADDININE NATUN FIL'AZAL A ZUCIYAR KOWANE JINJIRI, DA BAYANIN DABIAR DAN ADAM, AKWAI AMBATON AL'AJUBANA IKON ALLAH DA YAWA A CIKINTA, YANA DAGA CIKI BADA LABARIN GAIBU)

1.A.L.M. (Allahu-a'alamu-bi-muradihibi zalika. An rinjayi Rum (wato Farisa ta rinjayi Rum, su Rum ahlul kitabi ne, Farisa kuwa basu bane, sudai suna bautar gumaka ne, sai kafiran Makka sukayi farin ciki da wannan, sukace da Musulmi, "Mu zamu rinjayeku kamar yadda Farisa ta rinjayi Rum") **2.** a mafi kusancin ƙasar Rum izuwa Farisa a Jazira (wato tsakanin Dajlatu da Furatu wato ƙasar Iraƙi, wato Rumawa bayan an rinjayesu da sannu zasu rinjayi Farisa).

3. A cikin tsirarin shekaru (daga uku ko tara ko izuwa goma, sai yaƙi guda biyu ya haɗu wato yaƙin Kisra dayaƙin ƙaisara a shekara bakwai, daga gamuwa ta farko, sai Rumawa suka rinjayi Farisa).

4. Dukkan lamari ya tabbata ga Allah gaban (rinjayen Rum) da bayansa, a wannan rana (ranar da Rum tayi rinjaye) muminai zasuyifarin ciki.

وَعۡدَ ٱللَّهِۖ لَا يُخۡلِفُ ٱللَّهُ وَعۡدَهُۥ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ
لَا يَعۡلَمُونَ ﴿٦﴾ يَعۡلَمُونَ ظَٰهِرٗا مِّنَ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَهُمۡ
عَنِ ٱلۡأٓخِرَةِ هُمۡ غَٰفِلُونَ ﴿٧﴾ أَوَلَمۡ يَتَفَكَّرُواْ فِيٓ أَنفُسِهِمۗ
مَّا خَلَقَ ٱللَّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَآ إِلَّا بِٱلۡحَقِّ وَأَجَلٖ مُّسَمّٗىۗ
وَإِنَّ كَثِيرٗا مِّنَ ٱلنَّاسِ بِلِقَآيِٕ رَبِّهِمۡ لَكَٰفِرُونَ ﴿٨﴾ ۞ أَوَلَمۡ يَسِيرُواْ
فِي ٱلۡأَرۡضِ فَيَنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ
كَانُوٓاْ أَشَدَّ مِنۡهُمۡ قُوَّةٗ وَأَثَارُواْ ٱلۡأَرۡضَ وَعَمَرُوهَآ أَكۡثَرَ
مِمَّا عَمَرُوهَا وَجَآءَتۡهُمۡ رُسُلُهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِۖ فَمَا كَانَ ٱللَّهُ
لِيَظۡلِمَهُمۡ وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ﴿٩﴾ ثُمَّ كَانَ
عَٰقِبَةَ ٱلَّذِينَ أَسَٰٓـُٔواْ ٱلسُّوٓأَىٰٓ أَن كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ
وَكَانُواْ بِهَا يَسۡتَهۡزِءُونَ ﴿١٠﴾ ٱللَّهُ يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ
ثُمَّ إِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ﴿١١﴾ وَيَوۡمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ يُبۡلِسُ ٱلۡمُجۡرِمُونَ ﴿١٢﴾
وَلَمۡ يَكُن لَّهُم مِّن شُرَكَآئِهِمۡ شُفَعَٰٓؤُاْ وَكَانُواْ بِشُرَكَآئِهِمۡ كَٰفِرِينَ ﴿١٣﴾
وَيَوۡمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ يَوۡمَئِذٖ يَتَفَرَّقُونَ ﴿١٤﴾ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَهُمۡ فِي رَوۡضَةٖ يُحۡبَرُونَ ﴿١٥﴾

ربع

5. Da taimakon Allah garesu (a bisa Farisa, sunyi farin ciki da wannan, an sanar dasu a ranar daya afku a ranar Badar da saukowar Jibrila da wannan labari tareda farin cikinsu da nasarar -da suka samu a kan nushrikai) Allah yana taimakon wanda yaga dama, shine mabuwayi (ga kafirai) mai jinƙai (ga muminai).
6. Allah yayi musu alƙawarin taimako, Allah baya saɓa alƙawarinsa saidai yawancin mutane (kafiran Makka) basu san alƙawarin da Allah yayi (na taimakonsu ba).

(FANNONIN SANNAI WACCE CI GABAN DUNIYAYA RATAYA DA ITADA KAGE-KAGE SABABBI MASU BAN MANA KI)

7. Sunsan zahiri na rayuwar duniya (na aiki da noma da dashe da sauransu[1] su.kuwa rafkanannu ne su ga barin Lahira basa son komai nata ba.

(JAWO HANKALIN MASU HANKALI DA FIRGITA MUSHURIKAI. MUTUM SHINE AL'ALAMUL AKBAR, SAMMAI DA ƘASSAI SUNE AL'ALAMUL ASGARU)

8. Shin bazasuyi tunani a cikin kawukansu ba (donsu komo ga barin gafalarsu kuma donsu fahinci cewa mutum shinc Al'alamul Akbar, sama da ƙasa da Al'arshi sune Al'alamul asgar) Allah bai halicci sammai da ƙassaida abinda yake tsakaninsu basaida gaskiya da ajali abin ambato (ga wancananka, zata ƙare yayin ƙarewarsa da bayan tashi,) haƙiƙa yawaici daga mutane (kafiran Makka) lalle masu kafircewa ne da saduwa da Ubangijinsu (wato basu bada gaskiya da tashi bayan mutuwa ba).
9. Shin basuyi tafiya a cikin ƙasa basu duba yaya ƙarshen waɗanda suke gabansu (na daga al'umma? Itace an halakar dasu saboda ƙaryata manzanninsu) sun kasance mafiya ƙarfi daga garesu (kamar Adu da Samudu,) sun noma ƙasa sun gyaratada noma da dashe, mafi yawa yadda kafiran Makka suka gyarata manzanninsu sunzo musu da hujjoji mabayyana, Ubangiji bai tabbata donya zalince suba (da halakar dasu ba tareda laifi ba,) saidai sun kasance suna zaluntar kawukansune kawai (saboda ƙaryata manzanninsu).
10. Sannan ƙarshen waɗanda suka aikata mummunan aiki ta kasance mafi mummunar makoma (wato Jahannama,) saboda sun ƙaryatada ayoyin Allah (Alƙur'ani) sun kasance suna izgili da ita.
11. Allah shine mai fara halittar (mutane,) sannan ya mayar da halittarsu (bayan mutuwarsu) sannan izuwa gareshi ake komawa daku.
12. Ranar da Alƙiyama take tashi a rannan ake kwaɓe hanzarin mushurikai (saboda basu da hujja).
13. Kuma waɗansu sharikai basu kasance a garesu ba (wato gumaka masu ceto basu kasance garesu bana daga ababan tarayyar nasu) kuma zasu kasance masu kafircewa da gumakan nasu, (su barsu basu basu).
14. Ranar Alƙiyama a rannan ne suke tarwatsewa (muminai da kafirai).

1) Kamar ƙera jirgin sama da Atombom da talabijin na daga aikacc-aikaccn kimiyya - Sanagiy -

وَأَمَّا اَ۬لذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَلِقَآءِ اِ۬لَاخِرَةِ
فَأُوْلَٰٓئِكَ فِے اِ۬لْعَذَابِ مُحْضَرُونَ ﴿15﴾ فَسُبْحَٰنَ اَ۬للَّهِ حِينَ تُمْسُونَ
وَحِينَ تُصْبِحُونَ ﴿16﴾ وَلَهُ اُ۬لْحَمْدُ فِے اِ۬لسَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَعَشِيّاً
وَحِينَ تُظْهِرُونَ ﴿17﴾ يُخْرِجُ اُ۬لْحَيَّ مِنَ اَ۬لْمَيِّتِ وَيُخْرِجُ اُ۬لْمَيِّتَ
مِنَ اَ۬لْحَيِّ وَيُحْيِ اِ۬لْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَا وَكَذَٰلِكَ تُخْرَجُونَ ﴿18﴾
وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنْ خَلَقَكُم مِّن تُرَابٍ ثُمَّ إِذَآ أَنتُم
بَشَرٌ تَنتَشِرُونَ ﴿19﴾ وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنْ خَلَقَ لَكُم مِّنْ
أَنفُسِكُمْ أَزْوَٰجاً لِّتَسْكُنُوٓاْ إِلَيْهَا وَجَعَلَ بَيْنَكُم مَّوَدَّةً
وَرَحْمَةً إِنَّ فِے ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَتَفَكَّرُونَ ﴿20﴾
* وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦ خَلْقُ اُ۬لسَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَاخْتِلَٰفُ أَلْسِنَتِكُمْ ثمن
وَأَلْوَٰنِكُمْ إِنَّ فِے ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّلْعَٰلِمِينَ ﴿21﴾ وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦ
مَنَامُكُم بِالَّيْلِ وَالنَّهَارِ وَابْتِغَآؤُكُم مِّن فَضْلِهِۦٓ إِنَّ فِے ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ
لِّقَوْمٍ يَسْمَعُونَ ﴿22﴾ وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦ يُرِيكُمُ اُ۬لْبَرْقَ خَوْفاً
وَطَمَعاً وَيُنَزِّلُ مِنَ اَ۬لسَّمَآءِ مَآءً فَيُحْيِۦ بِهِ اِ۬لْأَرْضَ
بَعْدَ مَوْتِهَا إِنَّ فِے ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَعْقِلُونَ ﴿23﴾

15. Amma wađanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru, su ana faranta musu rai a cikin aljanna.
16. Amma wađanda suka kafirta suka ƙaryata ayoyinmu Alƙur'ani da saduwa da Lahira (tashi da waninsa) to wađannan ababan dauwamarwa ne a cikin azaba.

(TSARE SALLOLI BIYAR A CIKIN LOKATANSU BIYAR, TAREDA SAURAN ZIKIRAI DA WURIDAI A CIKIN WAĐANNAN LOKATAN)

17. Kuyi sallah ga Allah tareda ambatonsa lokacin da kuke shiga cikin sakaliyar dare wato (sallar magaribada lisha,) da lokacin da kuke shiga asuba, (wato sallar asuba kenan).
18. Yabo yana ga Allah cikin sammai da ƙassai (wato cikinsu shi suke yabo) da maraice, (wato sallar la'asar) dayayin da kuke shiga garjin rana (wato sallar azuhur).
19. Yana fitar da mai rai daga matacce (kamar mutum daga đigon majina ta maniyyi da tsuntsu daga ƙyanƙyashe ƙwai) yana fitar da matacce (maniyyi da ƙwai) daga rayayye, yana raya ƙasa (da tsiri) bayan ta ƙeƙashe. To, irin wannan fitarwar ake fitar daku (daga kaburbura).

(AYOYIN UBANGIJI DA GIRMAN KUDURARSA DA KADAITARSA DA RADDI GA WAĐANDASUKE CEWA MUTUM YA FARUNE DAGA BIRI DA BA'ALIN GARGADI)

20. Yana daga cikin ayoyin Ubangiji cewa ya halicce ku daga turbaya (wato asalinku Annabi Adamu alaihissalamu) to sai gakubilAdama daga jini da nama, kuna yađuwa a cikin ƙasa.
21. Yana daga cikin ayoyinsa cewa ya halicci mataye daga kawukanku donku, (Hawwa'u daga autan haƙarƙarin Annabi Adamu, sauran mata kuma daga đigon maniyyi na mazaje da mataye) domin ku nutsu izuwa gareta (ku sabada ita,) yasanyasoyayya da jinƙai a tsakaninku, haƙiƙa akwai ayoyi a cikin wancananka ga masu tunani (a cikin aikin Allah).
22. Yana daga cikin ayoyinsa halittar sammai da ƙassaida sabawar harasanku, (wato lugar da kuke magana na Larabci da baubauci da waninta) da launoninku (na daga fari da baƙi da waninsu, alhali ku 'ya'yan mutum đayane da mace đaya,) haƙiƙa akwai ayoyi cikin wancananka!
23. Yana daga ayoyinsa baccinku a cikin dare da rana (saboda nufinsa hutunku,) kuma da neman abincin rayuwarkuda rana, haƙiƙa akwai ayoyi cikin wancananka masu jin Alƙur'ani jin lura.

وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَن تَقُومَ ٱلسَّمَآءُ وَٱلْأَرْضُ بِأَمْرِهِۦۖ ثُمَّ إِذَا دَعَاكُمْ
دَعْوَةً مِّنَ ٱلْأَرْضِ إِذَآ أَنتُمْ تَخْرُجُونَ ﴿24﴾ وَلَهُۥ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِۖ كُلٌّ لَّهُۥ قَٰنِتُونَ ﴿25﴾ وَهُوَ ٱلَّذِے يَبْدَؤُاْ ٱلْخَلْقَ
ثُمَّ يُعِيدُهُۥ وَهُوَ أَهْوَنُ عَلَيْهِۖ وَلَهُ ٱلْمَثَلُ ٱلْأَعْلَىٰ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِۖ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿26﴾ ضَرَبَ لَكُم مَّثَلًا مِّنْ
أَنفُسِكُمْۖ هَل لَّكُم مِّن مَّا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُكُم مِّن شُرَكَآءَ
فِي مَا رَزَقْنَٰكُمْ فَأَنتُمْ فِيهِ سَوَآءٌ تَخَافُونَهُمْ كَخِيفَتِكُمْ أَنفُسَكُمْۖ
كَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلْآيَٰتِ لِقَوْمٍ يَعْقِلُونَ ﴿27﴾ بَلِ ٱتَّبَعَ
ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓاْ أَهْوَآءَهُم بِغَيْرِ عِلْمٍۖ فَمَنْ يَهْدِے مَنْ أَضَلَّ ٱللَّهُۖ
وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ﴿28﴾ فَأَقِمْ وَجْهَكَ لِلدِّينِ حَنِيفًاۖ فِطْرَتَ
ٱللَّهِ ٱلَّتِے فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيْهَاۖ لَا تَبْدِيلَ لِخَلْقِ ٱللَّهِۖ
ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلْقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ
لَا يَعْلَمُونَ ﴿29﴾ * مُنِيبِينَ إِلَيْهِ وَاتَّقُوهُ وَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ ربع
وَلَا تَكُونُواْ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿30﴾ مِنَ ٱلَّذِينَ فَرَّقُواْ دِينَهُمْ
وَكَانُواْ شِيَعًاۖ كُلُّ حِزْبِۢ بِمَا لَدَيْهِمْ فَرِحُونَ ﴿31﴾

24. Yana daga cikin ayoyinsa ya nuna muku walƙiya don tsoron (tsawa ga matafiya) da kuma sa tsammani (a cikin ruwa,) yana saukar da ruwa daga sama ya haƙiƙa Haƙiƙa raya ƙasa dashi bayan ƙeƙashewar ta, akwai ayoyin Ubangiji cikin wancananka ga mutane masu hankali.
25. Yana daga ayoyin Ubangiji sammai da ƙassaisu tsayaba tareda ginshiƙi basannan idan ya kirawo ku kira daga ƙasa (shine Mala'ika Israfilu yayi busa a cikin ƙaho don tashi daga kaburbura,) sai ga ku kuna fitowa daga gareta kuna rayayyu saboda fitowarkuda kira ɗaya. Yana daga ayoyin Ubangiji Ta'ala)
26. Dukan abinda ke cikin sammai da ƙassaina Allah ne, (mallaka da halittada bauta,) dukkan komai mai biyayya ne ga Allah.
27. Shine ya fara halittar mutane sannan ya mayar da halittar su (mutane) bayan sun mutu wannan shi yafi sauƙi gareshi dangane da al'adar mutane, amma inba haka ba ita halittar da tashin duk ɗayane a wajen Ubangiji.) Kyakkyawar siffa tana ga Ubangiji shine cewa ba abin bautawa da gaskiya sai Allah,) shine mabuwayi gwani (a cikin mulkinsa da halittarsa).

(KADAITAKAR UBANGIJI TA'ALA GA BARIN SHARIKI)

28. Ubangiji yasanya misali gareku yaku waɗannan mushurikai, mai kasancewa daga kanku, shine yalla kuna da wadansu abokan tarayya daga cikin abinda muka azurta ku dashi (nadaga dukiyoyi da waninta) a cikin abinda hannuwanku suka mallaka na daga ababan mallaka, to ku dasu madaidaita ne a cikinsa, kuna jin tsoronsu tamfar yadda kuke tsoron kawukanku, (wato 'ya'yaye irin ku, a'a, babu ababan tarayyagaremu a cikin ababan da muka mallaka, to yayakuke sa ba'alin abubuwan dasuke mallakar Allah ne kuke sanyasu abokan tarayyagareshi?) Kamar wancananka ne rarrabewa muke rarrabe ayoyi ga mutane masu hankali.
29. Ka bari! waɗanda suka zalinci kansu dashirka ga Ubangiji sunbi soye-soyen zukatansu bada ilimi ba, to wanene zai shiryi wanda Allah ya ɓatar dashi (babu,) basu da masu hana musu azabar Ubangiji.

(MUSULUNCI ADDININE NA HALITTAR ALLAH A ASALIN ƘIRAR 'YAN ADAM KUMA DA SHARUDDAN TAFARKUN SUFAYE)

30. Ka tsayar da mafuskantarka ga addini (Ya Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama) kana mai totar izuwa gareshi, (ai ka tsarkake addininka ga Allah kaida waɗanda sukabika,) ƙirar Allah ce wacce ya ƙera mutane a kanta, babu musayawa ga addinin Allah, (ma'ana kada kayi shirka,) wancananka shine addini madaidaici (tauhidin Allah,) saidai yawaicin mutane (kafiran Makka) basu san (tauhidin Allah ba).
31. Kuna masu komawa izuwa Allah (kai da waɗanda sukabika cikin abinda yayi umarni dashi da abinda yayi hani ga barinsa,) kuji tsoronsa, ku tsayar da sallah kadaku ,kasance daga cikin masu shirka ga Allah.

وَإِذَا مَسَّ النَّاسَ ضُرٌّ دَعَوْا رَبَّهُم مُّنِيبِينَ إِلَيْهِ ثُمَّ إِذَا أَذَاقَهُم
مِّنْهُ رَحْمَةً إِذَا فَرِيقٌ مِّنْهُم بِرَبِّهِمْ يُشْرِكُونَ (32) لِيَكْفُرُوا
بِمَا ءَاتَيْنَاهُمْ فَتَمَتَّعُوا فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ (33) أَمْ أَنزَلْنَا عَلَيْهِمْ
سُلْطَاناً فَهُوَ يَتَكَلَّمُ بِمَا كَانُوا بِهِ يُشْرِكُونَ (34) وَإِذَا أَذَقْنَا النَّاسَ
رَحْمَةً فَرِحُوا بِهَا وَإِن تُصِبْهُمْ سَيِّئَةٌ بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ
إِذَا هُمْ يَقْنَطُونَ (35) أَوَلَمْ يَرَوْا أَنَّ اللَّهَ يَبْسُطُ الرِّزْقَ لِمَن يَشَاءُ
وَيَقْدِرُ إِنَّ فِي ذَلِكَ لَآيَاتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ (36) فَـَٔاتِ ذَا الْقُرْبَى
حَقَّهُ وَالْمِسْكِينَ وَابْنَ السَّبِيلِ ذَلِكَ خَيْرٌ لِّلَّذِينَ يُرِيدُونَ وَجْهَ اللَّهِ
وَأُولَئِكَ هُمُ الْمُفْلِحُونَ (37) وَمَا ءَاتَيْتُم مِّن رِّباً لِّتُرْبُوا
فِي أَمْوَالِ النَّاسِ فَلَا يَرْبُوا عِندَ اللَّهِ وَمَا ءَاتَيْتُم مِّن زَكَوٰةٍ تُرِيدُونَ
وَجْهَ اللَّهِ فَأُولَئِكَ هُمُ الْمُضْعِفُونَ (38) اللَّهُ الَّذِي خَلَقَكُمْ ثُمَّ رَزَقَكُمْ
ثُمَّ يُمِيتُكُمْ ثُمَّ يُحْيِيكُمْ هَلْ مِن شُرَكَائِكُم مَّن
يَفْعَلُ مِن ذَلِكُم مِّن شَيْءٍ سُبْحَانَهُ وَتَعَالَى عَمَّا يُشْرِكُونَ (39)
* ظَهَرَ الْفَسَادُ فِي الْبَرِّ وَالْبَحْرِ بِمَا كَسَبَتْ أَيْدِي النَّاسِ
لِيُذِيقَهُم بَعْضَ الَّذِي عَمِلُوا لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ (40)

ثمن

32. Na daga waɗannan da suka rarraba addininsu ta wajen saɓaninsu dayadda suke bauta masa suka zama dabam-daban, dukkan ƙungiya suna masu farin ciki da abinda yake gunsu.

(BAYANIN DABI'AR MUTANE TAREDA FUSKANTARWAR UBANGIJI GARESU KATANGAR SHIRIYA)

33. Idan tsanani ya sami mutane, (wato kafiran Makka) saisu ɗora kiran Ubangijinsu suna masu komawa gareshi shi kaɗai ba tareda waninsa ba, sannan idan ya ɗanɗana musujinƙai daga gareshi (wato ruwa) sai gasu suna shirkantawa dashi.
34. To su kafirtada abinda muka basu ɗin (wannan ban tsoro ne daga Allah) kuci gabada jin daɗin, da sannu zaku ga ƙarshen jin daɗinku.
35. Shin mun saukar musu da hujja ne da littafi? Shi littafin nan ya zama yana zantar dasu abinda suka kasance suna shirkantawa (wato ma'ana ya umarce su dashirka, a'a.)
36. Idan muka ɗanɗanawa kafiran Makka da wasunsu rahama sai suyi murna da ita, murna ta girman kai, idan tsanani ya samesu saboda abinda hannuwansu ta gabatar sai gasu suna ɗebe haso daga rahamar Ubangiji (yana daga sha'anin mumini yayi godiya yayin ni'ima, ya ƙaunaci yayewa yayin tsanani)
37. Shin basu sani cewa Allah yana yalwatawar arziki ga wanda yaga dama bane (don gwadawa gareshi), yana ƙuntatawa ga wanda yaga dama (don gwadawa gareshi) haƙiƙa akwai ayoyi cikin wancananka ga mutane masu bada gaskiya (da ita).
38. To saika baiwa ɗan uwan zumuncinka haƙƙinsa (na daga kyautawa da sadar da zumunta,) da musaki da matafiyi daga cikin sadaka, (al'ummar ma'aiki masu bine gareshi cikin wannan,) wancananka shine yafi ga waɗanda suke nufin sakamakon zatin Ubangiji, waɗancananka sune haƙiƙanin marabauta.
39. Abinda duk zaku bayar na daga riba (wato ɓatanci daya shafi daɗi shine mutum ya bada wata kyauta ko hadiya saboda neman mafi yawa daga shi, an ambace shi abin nema na daga ƙari a cikin ma'amala,) donya daɗu a cikin dukiyoyin mutane (waɗanda aka basu,) to bazai tsarkake ba nan ga Allah (wato ba lada cikinsa,) abinda zaku bayar (wato na daga zakka ko sadaka kuna nufin Zatin Allah da ita. Wadancananka sune masu ninninka sakamakonsu.

(WANI ABU NA DAGA DALILAN TAUHIDI DA NATIJOJIN AYYUKA 'WATO AMFANIN AYYUKA')

40. Allah ne wanda ya halicce ku sannan ya azurta ku, sannan ya karɓi ranku, sannan zai rayaku. Akwai daga wanda kuka shir-kantashi da Allah wandazai aikata wani abu daga wancananku? (Babu). Tsarki ya tabbatar masa ya girmama ga barin abinda kuke shirkantashi dashi.

(KOMAI YA SAMEMU A DUNIYAKUDARMU MUKE DANDANAWA)

Ubangiji ya ɗanɗana muku abinda suka aikata (ai sakamakonsa) saboda su tuba ga Allah.

قُلْ سِيرُواْ فِي اِ۬لْأَرْضِ فَانظُرُواْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ اُ۬لذِينَ مِن قَبْلُۖ
كَانَ أَكْثَرُهُم مُّشْرِكِينَۖ (41) فَأَقِمْ وَجْهَكَ لِلدِّينِ اِ۬لْقَيِّمِ مِن قَبْلِ
أَن يَّأْتِيَ يَوْمٞ لَّا مَرَدَّ لَهُۥ مِنَ اَ۬للَّهِۖ يَوْمَئِذٖ يَصَّدَّعُونَۖ (42) مَن كَفَرَ
فَعَلَيْهِ كُفْرُهُۥۖ وَمَنْ عَمِلَ صَٰلِحاٗ فَلِأَنفُسِهِمْ يَمْهَدُونَ (43)
لِيَجْزِيَ اَ۬لذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ اُ۬لصَّٰلِحَٰتِ مِن فَضْلِهِۦٓۖ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ اُ۬لْكَٰفِرِينَۖ (44)
وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَن يُّرْسِلَ اَ۬لرِّيَاحَ مُبَشِّرَٰتٖ وَلِيُذِيقَكُم مِّن رَّحْمَتِهِۦ
وَلِتَجْرِيَ اَ۬لْفُلْكُ بِأَمْرِهِۦ وَلِتَبْتَغُواْ مِن فَضْلِهِۦ وَلَعَلَّكُمْ
تَشْكُرُونَۖ (45) وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ رُسُلاً إِلَيٰ قَوْمِهِمْ
فَجَآءُوهُم بِالْبَيِّنَٰتِ فَانتَقَمْنَا مِنَ اَ۬لذِينَ أَجْرَمُواْۖ وَكَانَ حَقّاً
عَلَيْنَا نَصْرُ اُ۬لْمُؤْمِنِينَۖ (46) اَ۬للَّهُ اُ۬لذِي يُرْسِلُ اُ۬لرِّيَاحَ فَتُثِيرُ سَحَاباٗ
فَيَبْسُطُهُۥ فِي اِ۬لسَّمَآءِ كَيْفَ يَشَآءُ وَيَجْعَلُهُۥ كِسْفاٗ فَتَرَى اَ۬لْوَدْقَ يَخْرُجُ
مِنْ خِلَٰلِهِۦۖ فَإِذَا أَصَابَ بِهِۦ مَن يَّشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦٓ إِذَا هُمْ يَسْتَبْشِرُونَۖ (47)
وَإِن كَانُواْ مِن قَبْلِ أَن يُنَزَّلَ عَلَيْهِم مِّن قَبْلِهِۦ لَمُبْلِسِينَۖ (48)
فَانظُرِ إِلَيٰ أَثَرِ رَحْمَتِ اِ۬للَّهِ كَيْفَ يُحْيِ اِ۬لْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَاۖ
إِنَّ ذَٰلِكَ لَمُحْيِ اِ۬لْمَوْتَيٰۖ وَهُوَ عَلَيٰ كُلِّ شَيْءٖ قَدِيرٞۖ (49)

41. Sakamakon ƙarna ya bayyana a cikin sarari (fari na ruwa da ƙarancin abinci da kogi (wato garuruwa wacce take a gefen kogi da ƙarancin ruwanta,) saboda abinda hannuwan mutane suka gabatar, (na daga saɓanin Ubangijj,) saboda

42. Cene (ga kafiran Makka) "Kuyi tafiya a cikin ƙasa to ku duba yaya ƙarshen waɗanda suke gabaya kasance, yawaicinsu sun kasance mushurikai (sai aka halakar dasu saboda mushurikancinsu da gidaddajinsu ba kowa) a ciki.

43. Ka tsayar da fuskarka ga addinin Musulunci tun gaban rana batazo ba wadda ba makawa (Itace ranar alkiyama,) a wannan rana zasu tarwatse (izuwa aljanna ko wuta).

44. Wanda ya kafirta, to kafirci na gareshi, wanda yayi aiki na gari suna yin shimfiɗa ne ga kawukansu, (suna shirya masaukansu).

45. (Zasu tarwatse) saboda Ubangiji ya sakawa waɗanda sukayi nagargaru daga falalarsa, zaiyi musu sakamako, Ubangiji bayason kafirai (uƙuba yake musu).

(WANI ABU DAGA AYOYIN UBANGIJI NA ISKA DA RUWA)

46. Yana daga ayoyinsa ya aiko da iskoki masu albishir da ruwa don tayi muku albishir (da ruwa) kuma ya ɗanɗana muku daga rahama tasa ruwa da kaka,kuma saboda jiragasu gudana da umarnin Ubangiji kuma sabodaku ,nema daga falalar Allah (wato da fatauci a cikin kogi ana) ƙaunar kwa godewa ni'imar Ubangiji gareku (yaku mutanen Makka wato ku kaɗaita Ubangiji).

47. Haƙiƙa mun aiko manzanin gabanka izuwa mutanensu, sukazo musu da hujjoji mabayyana (a kan gaskiyarsu a cikin aikosu izuwa garesu,) suka ƙaryata su, sai mukayi damƙa daga waɗanda sukayi zunubi, muka halakar dasu, ya tabbata lallene a kammu taimakonmu ga muminai a kan kafirai (mu halakar da kafirai mu tserar da muminai).

48. Allah shine wanda yake aiko iskoki su motso giza gizai ya shimfiɗe shi a cikin sama irin yadda yaga dama na daga yawa ko ƙanƙanta, Ya sanyashi yanki yanki saika dinga hangen ruwa yana fitowa daga tsatstsakinsa, idan yasami wanda yaga dama daga bayinsa, sai gasu suna farin ciki da samun ruwa.

49. Haƙiƙa sun kasance gaban ba a saukar (dashi a garesu ba, lalle suna deɓe haso) daga saukarsa.

وَلَئِنْ أَرْسَلْنَا رِيحاً فَرَأَوْهُ مُصْفَرّاً لَّظَلُّواْ مِنۢ بَعْدِهِۦ يَكْفُرُونَ ﴿50﴾
فَإِنَّكَ لَا تُسْمِعُ الْمَوْتَىٰ وَلَا تُسْمِعُ الصُّمَّ الدُّعَآءَ إِذَا وَلَّوْاْ مُدْبِرِينَ ﴿51﴾
وَمَا أَنتَ بِهَٰدِ الْعُمْيِ عَن ضَلَٰلَتِهِمُۥٓ إِن تُسْمِعُ إِلَّا مَن يُؤْمِنُ بِـَٔايَٰتِنَا
فَهُم مُّسْلِمُونَ ﴿52﴾ ۞ اللَّهُ الَّذِے خَلَقَكُم مِّن ضُعْفٍ ثُمَّ جَعَلَ مِنۢ بَعْدِ ضُعْفٍ (ربع)
قُوَّةً ثُمَّ جَعَلَ مِنۢ بَعْدِ قُوَّةٍ ضُعْفاً وَشَيْبَةً يَخْلُقُ مَا يَشَآءُ
وَهُوَ الْعَلِيمُ الْقَدِيرُ ﴿53﴾ وَيَوْمَ تَقُومُ السَّاعَةُ يُقْسِمُ
الْمُجْرِمُونَ ﴿54﴾ مَا لَبِثُواْ غَيْرَ سَاعَةٍ كَذَٰلِكَ كَانُواْ يُؤْفَكُونَ ﴿55﴾
وَقَالَ الَّذِينَ أُوتُواْ الْعِلْمَ وَالْإِيمَٰنَ لَقَدْ لَبِثْتُمْ
فِے كِتَٰبِ اللَّهِ إِلَىٰ يَوْمِ الْبَعْثِ فَهَٰذَا يَوْمُ الْبَعْثِ وَلَٰكِنَّكُمْ
كُنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴿56﴾ فَيَوْمَئِذٍ لَّا تَنفَعُ الَّذِينَ ظَلَمُواْ
مَعْذِرَتُهُمْ وَلَا هُمْ يُسْتَعْتَبُونَ ﴿57﴾ وَلَقَدْ ضَرَبْنَا لِلنَّاسِ
فِے هَٰذَا الْقُرْءَانِ مِن كُلِّ مَثَلٍ وَلَئِن جِئْتَهُم بِـَٔايَةٍ لَّيَقُولَنَّ
الَّذِينَ كَفَرُواْ إِنْ أَنتُمْ إِلَّا مُبْطِلُونَ ﴿58﴾ كَذَٰلِكَ
يَطْبَعُ اللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِ الَّذِينَ لَا يَعْلَمُونَ ﴿59﴾ فَاصْبِرْ
إِنَّ وَعْدَ اللَّهِ حَقٌّ وَلَا يَسْتَخِفَّنَّكَ الَّذِينَ لَا يُوقِنُونَ ﴿60﴾

50. Sai kayi duba izuwa gurbin rahamar Allah da saukar ruwa, yayaya raya ƙasa bayan ƙeƙashewarta, haƙiƙa wancananka (wanda ya raya ƙasa) lalle mai raya matattune, kuma shine mai iko bisa komai.
51. haƙiƙa, Wallahi inmun aiko iska bakarara (wacce bata haifa girgije ayan kwane bata fitar da amfani daga tsiri,) ta motso girgije suka ganshiya shimfiɗe shi asama irin yadda yaga dama na daga ƙaranci ko yawa yasanya giza gizai sai kaga ruwa yana fita daga tsatstsakinsa, idan yasami Wanda yaga dama na bayinsa daga Wannan ruwa Sai gasu suna farin ciki dashi dacanko kun kasance gaban saukarsa agaresu fun gabansa masu debe haso daga saukarsa) bayannan saisu zama suna kafircewa da ni'imar Ubangiji (wato ta ruwa).
52. Haƙiƙa kai baka jiyar da matattu baka jiyar da kurame kira idan sun girka aguje da baya.
53. Kai baka shiryar da makafi ga barin ɓatansu baka jiyarwa sai wanda ya bada gaskiya da ayoyinmu (Alƙur'ani) sune Musulmi (masu tsarkake Ubangiji

(AL'AJABAN UBANGIJI A CIKIN BIL-ADAMA DA ZAMANSA MAI BAYYANA FALALAR ALLAH DA ADALCINSA)

54. Ubangiji shine wanda ya halicceku daga rauni (wato ruwa wulaƙantacce,) sannan bayan wani rauni daban (wato raunin jarirantaka yasanya ƙarfi wato ƙarfin samartaka) sannan bayan wani ƙarfin yasanya rauni da furfura. Yana halittar abinda yaga dama, (na rauni da ƙuruciya da furfura,) Ubangiji shine masani (dashirin halittarsa) mai iko (bisa abinda yaga dama).
55. Ranar Alƙiyama kafirai zasu rinƙa rantsuwa basu zauna a cikin kaburbura basai sa'a ɗaya, don haka nan ana juyar dasu ga barin gaskiya, (wato tashin Alƙiyama tamfar yadda ake juyar dasu ga barin gaskiya muddar zamansu a cikin ƙaburbura).
56. waɗanda suke da ilimi da imani na Mala'ikuda wasunsu sukace "Lalle kun zauna izuwa ranar Alƙiyama, to, wanna Itace ranar Alƙiyama (wadda kuke musun ta,) saidai ku kun kasance baku san afkuwarta ba!
57. A wannan rana hanzarin waɗanda sukayi zalunci (da kafirci) bazai amfanesu ba, (a cikin musunsu da wannan rana) kuma baza a nemesu da abindazai komo dasu izuwa abindazai yardar da Allah ba.
58. Haƙiƙa mun sanyaga mutane daga kowane misali cikin wannan alƙur'ani (don faɗakarwa garesu,) Wallahi inka zomusu da aya (Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama) misalin sanda da hannun Annabi Musa alaihissalamu, lalle waɗanda suka kafirta zasuce ku (Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama da Sahabbansa) baku zamo ba illa maɓarnata (ma'abota ƙaryace -ƙaryace).
59. (Kamar yadda Allah ya yimƙe bisa zukatan waɗannan,) haka yake yimƙewar bisa zukatan waɗanda basusan tauhidi ba.
60. To haƙura, haƙiƙa alƙawarin Allah (da taimako a kansu) tabbatacce ne, to waɗanda basu sakankance da tashin alƙiyama ba to kadasuyi wasada hankalinka.

سُورَةُ لُقْمَانَ مَكِّيَّةٌ 31

وَهِيَ ثَلَاثٌ وَثَلَاثُونَ ءَايَةً 33

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓمٓ تِلْكَ ءَايَٰتُ ٱلْكِتَٰبِ ٱلْحَكِيمِ (1) هُدًى وَرَحْمَةً لِّلْمُحْسِنِينَ (2)
ٱلَّذِينَ يُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤْتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَهُم بِٱلْءَاخِرَةِ هُمْ يُوقِنُونَ (3)
أُوْلَٰٓئِكَ عَلَىٰ هُدًى مِّن رَّبِّهِمْ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ (4) وَمِنَ ٱلنَّاسِ
مَن يَشْتَرِي لَهْوَ ٱلْحَدِيثِ لِيَضِلَّ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ بِغَيْرِ عِلْمٍ وَيَتَّخِذُهَا
هُزُؤًا أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمْ عَذَابٌ مُّهِينٌ (5) وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِ ءَايَٰتُنَا
وَلَّىٰ مُسْتَكْبِرًا كَأَن لَّمْ يَسْمَعْهَا كَأَنَّ فِي أُذْنَيْهِ وَقْرًا فَبَشِّرْهُ
بِعَذَابٍ أَلِيمٍ (6) إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا وَعَمِلُوا ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُمْ جَنَّٰتُ
ٱلنَّعِيمِ (7) خَٰلِدِينَ فِيهَا وَعْدَ ٱللَّهِ حَقًّا وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ
ٱلْحَكِيمُ (8) خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ بِغَيْرِ عَمَدٍ تَرَوْنَهَا وَأَلْقَىٰ
فِي ٱلْأَرْضِ رَوَٰسِيَ أَن تَمِيدَ بِكُمْ وَبَثَّ فِيهَا مِن كُلِّ دَآبَّةٍ وَأَنزَلْنَا مِنَ
ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَنۢبَتْنَا فِيهَا مِن كُلِّ زَوْجٍ كَرِيمٍ (9) هَٰذَا خَلْقُ ٱللَّهِ
فَأَرُونِي مَاذَا خَلَقَ ٱلَّذِينَ مِن دُونِهِۦ بَلِ ٱلظَّٰلِمُونَ فِي ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ (10)

Suratu Lukmanu

A Makka Aka. Saukar Da Ita Ayoyinta Talatin Da Uku (33)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

(ITA WANNAN SURA TA TARA MUHIMMAN AL'AMURA NA TASHIN ALƘIYAMA DA WAHADINIYAR UBANGIJI DA GASKIYAR MANZONCINSA (S.A-W) DA MASU KAFIRCEWA DA ALƘUR'ANI, DA MASU BADA GASKIYA DASHI) 'TASIRIN ALƘUR'ANI A ZUKATAN MUSULMI'

1. A.L.M. Allahu a'alamu bi muradihi-bizalika. (Allah shine mafi sani da abinda yake nufi da wancananka). Waɗannan ayoyin littafine mai hikima (Alƙur'ani).
2. Shi shiriyane da jinƙai ga masu Ihsani (wato masana Allah).
3. Sune waɗanda suka tsayar da salla daidai-wa-daidasuke bada zakka, su masu sakankancewa ne (da tashin Alƙiyama, su masu sakankancewa ne da ranar Lahira).
4. Waɗancananka sun tabbata a kan shiriya daga Ubangijinsu, waɗancananka sune marabauta (na haƙiƙa).

(MAKAFIRTADA ƘUR'ANI DA MASU BADA GASKIYA DASHI)

5. Akwai daga mutane wanda yake sayen maganar wasanni abinda yake zai shagalar dashi ga barin abindazai amfane shi,) donya ɓatar da (mutane) ga barin hanyar Musulunci bada sani ba yake riƙonta abin izgili da ita.Waɗancananka azaba mai wula-ƙantarwa ta tabbata garesu.
6. Idan ana karanta ayoyinmu a gareshi saiya bada baya yana mai girmankai, kamar bai taɓa jin taɓa, kai kace akwai kummta a kunnuwansa guda biyu. To. yi masa albishir da azaba mai raɗaɗi.
7. Haƙiƙa waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru, aljannatai na ni'ima na garesu.
8. Masu dauwama a cikinta, Ubangiji ya alƙawarta wannan alƙawartarwa (ya tabbatar dashi tabbatarwa) shine mabuwayi mai hikima.

(WANNAN HALITTAR ALLAH NE) HAƘIƘA MUHAMMADIYYA DA HASKEN MANZON ALLAH SALLAL LAHU ALAIHI WASSALLAMA, UBANGIJI YA TOKARE SAMMAI DASHI DA SAURAN KA'INATU. SHINE AL - HIJABUL A' AZAM.

9. Allah ya halicci sammai bada ginshiƙai da kuke ganinta ba (yana yiwuwa ba ginshiƙin kwatakwata, yana yiwuwa da ginshiƙin wanda bakwa gani,) ya kafa duwatsu a cikin ƙasa don kada tayi motsi daku, ya daidaita a cikinta daga dukkan dabba mai motsi ya saukar da ruwa daga sama, ya tsiro da nau'i kyakkyawa daga ƙasa [1]
10. To, wannan halittar Allah ne, to ku nuna min abinda waɗanda suke ba Allah basukayi, bari azzalumai dai suna cikin ɓata mabayyani.

1) Wanda Imamu Muslim yake cewa hijabin Ubangiji haskene, dazai yayeshi da zafin Haskake - HasKaken Zatinsa sun Rone abinda ya sadu dashi na daga halittarsa shine kuna : (Atamadulazi la yura). - Sanajiy -

ثمن

* وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا لُقْمَٰنَ اَلْحِكْمَةَ أَنُ اِشْكُرْ لِلَّهِ وَمَنْ يَّشْكُرْ
فَإِنَّمَا يَشْكُرُ لِنَفْسِهِۦ وَمَن كَفَرَ فَإِنَّ اَللَّهَ غَنِيٌّ حَمِيدٌ ﴿11﴾
وَإِذْ قَالَ لُقْمَٰنُ لِابْنِهِۦ وَهْوَ يَعِظُهُۥ يَٰبُنَيِّ لَا تُشْرِكْ بِاللَّهِ
إِنَّ اَلشِّرْكَ لَظُلْمٌ عَظِيمٌ ﴿12﴾ وَوَصَّيْنَا اَلْإِنسَٰنَ بِوَٰلِدَيْهِ حَمَلَتْهُ
أُمُّهُۥ وَهْنًا عَلَىٰ وَهْنٍ وَفِصَٰلُهُۥ فِي عَامَيْنِ أَنُ اِشْكُرْ لِي وَلِوَٰلِدَيْكَ
إِلَيَّ اَلْمَصِيرُ ﴿13﴾ وَإِن جَٰهَدَاكَ عَلَىٰٓ أَن تُشْرِكَ بِي مَا لَيْسَ لَكَ بِهِۦ عِلْمٌ
فَلَا تُطِعْهُمَا وَصَاحِبْهُمَا فِي اِلدُّنْيَا مَعْرُوفًا وَاتَّبِعْ سَبِيلَ
مَنْ أَنَابَ إِلَيَّ ثُمَّ إِلَيَّ مَرْجِعُكُمْ فَأُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿14﴾
يَٰبُنَيِّ إِنَّهَا إِن تَكُ مِثْقَالُ حَبَّةٍ مِّنْ خَرْدَلٍ فَتَكُن فِي صَخْرَةٍ
أَوْ فِي اِلسَّمَٰوَٰتِ أَوْ فِي اِلْأَرْضِ يَأْتِ بِهَا اَللَّهُ إِنَّ اَللَّهَ
لَطِيفٌ خَبِيرٌ ﴿15﴾ يَٰبُنَيِّ أَقِمِ اِلصَّلَوٰةَ وَأْمُرْ بِالْمَعْرُوفِ وَانْهَ
عَنِ اِلْمُنكَرِ وَاصْبِرْ عَلَىٰ مَا أَصَابَكَ إِنَّ ذَٰلِكَ مِنْ عَزْمِ اِلْأُمُورِ ﴿16﴾
وَلَا تُصَٰعِرْ خَدَّكَ لِلنَّاسِ وَلَا تَمْشِ فِي اِلْأَرْضِ مَرَحًا إِنَّ اَللَّهَ
لَا يُحِبُّ كُلَّ مُخْتَالٍ فَخُورٍ ﴿17﴾ وَاقْصِدْ فِي مَشْيِكَ وَاغْضُضْ
مِن صَوْتِكَ إِنَّ أَنكَرَ اَلْأَصْوَٰتِ لَصَوْتُ اُلْحَمِيرِ ﴿18﴾

(ƘISSAR ANNABI LUKMANU DA WASIYYARSA GA DANSA WAƊANDASUNE SHARUDDAN SHEHUNAN DARIKA GA MURIDANSU MAGASGATA)

11. Haƙiƙa mun baiwa Lukmanu hikima. hikima (kamar ilimi da kula da addini da dacewa a cikin magana, hikimominsa waɗanda aka ruwaito suna da yawa, ya kasance yana fatawa gaban aiko Annabi Dawuriu ya riski aikoshiya karɓi ilimi a gurinsa. Annabi Luƙmanu ya daina fatawa yace; "Bana huta ba idan an hutar dani?" Ance dashi wannene daga mutane yafi sharri, yace, wanda bai kula ba in mutane sun ganshi yana mai munanawa) Munce dashi godewa Allah bisa abinda yabaka na daga hikima, duk wanda ya godewa ni'imar Allah) to ya godene ga kansa kawai, domin ladan godiyar tasa nasa ne. Duk wanda ya butulcewa ni'imar Allah haƙiƙa Ubangiji mawadaci ne ga barin halittarsa, abin godewa ne cikin aikinsa.
12. Ka ambata zamanin da Luƙmanu alhakimi ya faɗa ga ɗansa, alhali yanayi masa wa'azi, yace, "Ya ƙaramin ɗana kada kayi shirka da Allah, haƙiƙa shirka da Allah lalle zalinci ne mai girma". (Yakoma izuwa gareshiya Musulunta).
13. Munyiwa mutum wasiyya da bin iyayensa (mun umarceshi yayi biyayya a garesu) mahaifiyarsa ta ɗauki cikinsa ta raunana rauni kan rauni, (tayi rauni saboda ciki, tayi rauni saboda haihuwa) tayaye shi a cikin shekara biyune, (munce dashi) "godemin kuma ka godewa mahaifanka, kyakkyawar makoma ta tabbata gurina".
14. Idan sun yaƙeka a kan ka shirkanta damu a kan abinda bakada sani dashi, to kada kabisu, kaidai ka abucesu da alheri a duniya da sadar da zumunta) kabi tafarkin wanda yayi biyayya ga reni, sannan izuwa gareni makomarku take, inbaku labarin abinda kuka kasance kuna aikatawa (inyi muku sakamako agareshi)".
15. Yakai ƙaramin ɗana, haƙiƙa al'amari inta kasance misalin ƙwaya ta komayya ta kasance cikinta, ko a cikin sammai ko a cikin ƙassai Allah zaizoda ita (yayi hisabi a kanta, wannan fa tana cikin mafi ɓuyan guri,) haƙiƙa Ubangiji masanine da ɓoyayyun al'amura dayasan zahirin ta (ance wannan kalma Itace kalmar da Luƙmanu yayi magana da ita, sai matsarmana r ɗansa ta kyakkece saiya mutu yana Musulmi, shahidi).
16. Yakai ɗan ƙaramin ɗana, ka tsayar da salla daidai-wadaida, kayi umarni da aikin alheri, kayi hani ga aikin munkari, kadaure bisa abinda ya sameka (saboda amru da nahyu) haƙiƙa wancananka (abin ambato) yana daga cikin matsanantan manyan al'amura (Waɗanda Allah yayi umarni da a yisu).
17. Kadaka fizge fuskarka ga barin mutane don girmankai, kada kayi tafiya a bayan ƙasa kana taƙama, haƙiƙa Allah bayason dukkan mai taƙama a cikin tafiyarsa mai fariya (a kan mutane).
18. Ka tsakaita a cikin tafiyarka (tsakanin dudduke da gaggawa, katafi a cikin nutsuwa) ka runtse muryarka, haƙiƙa mafi munin muryoyi lalle muryar jaki, (farkonsa amo, ƙarshensa sheshsheƙa, kuma babu ambaton Allah a cikin muryarsa kamar yadda Allah yabada shaida a kan haka, Sawi).

ألم تروا أن الله سخر لكم ما في السموات وما في الأرض
وأسبغ عليكم نعمه ظاهرة وباطنة ومن الناس من يجادل
في الله بغير علم ولا هدى ولا كتاب منير ﴿19﴾ وإذا قيل لهم
اتبعوا ما أنزل الله قالوا بل نتبع ما وجدنا عليه ءاباءنا
أولو كان الشيطان يدعوهم إلى عذاب السعير ﴿20﴾ * ومن يسلم
وجهه إلى الله وهو محسن فقد استمسك بالعروة الوثقى
وإلى الله عاقبة الأمور ﴿21﴾ ومن كفر فلا يحزنك كفره إلينا
مرجعهم فننبئهم بما عملوا إن الله عليم بذات الصدور ﴿22﴾ نمتعهم
قليلا ثم نضطرهم إلى عذاب غليظ ﴿23﴾ ولئن سألتهم من خلق السموات
والأرض ليقولن الله قل الحمد لله بل أكثرهم
لا يعلمون ﴿24﴾ لله ما في السموات والأرض إن الله
هو الغني الحميد ﴿25﴾ ولو أنما في الأرض من شجرة
أقلام والبحر يمده من بعده سبعة أبحر ما نفدت
كلمات الله إن الله عزيز حكيم ﴿26﴾ ما خلقكم
ولا بعثكم إلا كنفس واحدة إن الله سميع بصير ﴿27﴾

حزب

(GODEWAMAI NI'IMTAWA WAJIBINE A SHARI'A DA HANKALI DA AL'ADA)

19. Shin baku saniba (yaku abokan zance?) Haƙiƙa Allah ya hore muku abinda ke cikin sammai (na daga rana da watada taurari domin kuyi amfani dashi) da abinda yake cikin ƙassai) na daga 'ya'yan itatuwa da dabbobi da sauransu) ya cika ni'imominsa a gareku na zahiri (kamar kyan sura da daidaituwar gaɓuɓuwa da wanin wancananka) dana baɗini (Itace sanin Allah da sanin Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama da waninta,) akwai daga mutanen Makka wanda yake jayayya da sha'anin Allah bada ilimi ba badashiriya (daga manzo) ba bada littafi mai haske ba (wanda Allah ya saukar).
20. In ance dasu "Kubi abinda Allah ya saukar", sai suce, "Zamubi abinda muka sami iyayenmu a kansa, shin (sabishi) koda shaiɗan yana kiransu izuwa wuta? (A'a, basabin abinda suka sami iyayensu a kansa ba,sudai zasuyi kwaikwayone a cikin abubuwa na gargaru waɗanda Allah ko ma'aikin Allah suka yabadasu ko malamai na Allah suka yabadasu).

(MASU CIKAKKEN IMANI DA WANINSU)

21. Duk wanda ya miƙa kulliyarsa izuwa Allah (a bisa da'arsa,) alhali shi mai sakankancewane da Allah (da kaɗaitawa gareshi,) to haƙiƙa yayi riƙo da igiya mafi aminci wadda ba a tsoron yankewarta, ƙarshen al'amurra duka ya tabbata ga Allah.
22. Wanda ya kafirta to kada kafirtarsa ta baƙanta maka, izuwa garemu komowarsu take, mubasu labari da abinda suka aikata (wato muyi musu sakamako) haƙiƙa Ubangiji masanine da abinda yake ƙirazan bayi (zaiyi sakamako a kansa.)
23. Muna jiyar dasu daɗi kaɗan (a duniya kwanukan rayuwarsu) sannan mu buƙatar dasu a Lahira izuwa azaba mai kauri (shine azabar wuta, baza a sami makardada ga barinsu ba!)

(GIRMAN ALLAH MAHALICCI DA AMBATON AYOYINSA)

24. Wallahi inka tambayesu waya halicci sammai da ƙassai lalle zasuce maka "Allah ne", cene "Godiya ta tabbata ga Allah (a bisa rinjayen hujja kansu da tauhidi,) kai yawancinsu basu san (wajabcin tauhidi a kansu ba).
25. Abinda yake cikin sammai da ƙassaina Allah ne (mallaka da halittada bauta, ba wanda ya cancanci bauta a cikinsu sai shi), haƙiƙa Ubangiji shine mawadaci (ga barin halittarsa,) abin godewa (a cikin aikinsa.)
26. Dadai cewa abinda ke cikin duniya na daga itatuwa alƙalumane da kogi mai kewayewa koguna guda bakwai suna karinsa bayan shi kansa, (wato ko suna ruwan tauwada) kalmomin Allah bazasu kareba, (wanda ake fassara da ita ga ababan sanin Allah ta wajen rubutatada wancananka alƙaluma da wancananka tauwada wala da mafi yawa daga wancananka, domin ababan sanin Allah ta'ala bamai tiƙewane ba,) haƙiƙa Ubangiji mabuwayi ne (ba abinda yake gajishe shi,) gwanine (ba abinda yake fita ga barin iliminsa da hikimarsa.)
27. Halittarkuda tashinku basu kasance ba illa kamar halittar kai ɗaya (saboda shi da kalmar KUN FA YAKUNU ce) haƙiƙa Ubangiji maijine (ga dukkan abinji) mai ganine (ga dukkan abin gani, wani abu baya shagalar dashi ga barin wani abu).

أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ يُولِجُ ٱلَّيۡلَ فِي ٱلنَّهَارِ وَيُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِي ٱلَّيۡلِ
وَسَخَّرَ ٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَ كُلٌّ يَجۡرِيٓ إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمّٗى وَأَنَّ ٱللَّهَ
بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٞ ﴿٢٨﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡحَقُّ وَأَنَّ مَا يَدۡعُونَ
مِن دُونِهِ ٱلۡبَٰطِلُ وَأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡعَلِيُّ ٱلۡكَبِيرُ ﴿٢٩﴾ أَلَمۡ تَرَ
أَنَّ ٱلۡفُلۡكَ تَجۡرِي فِي ٱلۡبَحۡرِ بِنِعۡمَتِ ٱللَّهِ لِيُرِيَكُم مِّنۡ ءَايَٰتِهِۦٓۚ
إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّكُلِّ صَبَّارٖ شَكُورٖ ﴿٣٠﴾
* وَإِذَا غَشِيَهُم مَّوۡجٞ كَٱلظُّلَلِ دَعَوُاْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ
فَلَمَّا نَجَّىٰهُمۡ إِلَى ٱلۡبَرِّ فَمِنۡهُم مُّقۡتَصِدٞۚ وَمَا يَجۡحَدُ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَّا
كُلُّ خَتَّارٖ كَفُورٖ ﴿٣١﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱتَّقُواْ رَبَّكُمۡ
وَٱخۡشَوۡاْ يَوۡمٗا لَّا يَجۡزِي وَالِدٌ عَن وَلَدِهِۦ وَلَا مَوۡلُودٌ
هُوَ جَازٍ عَن وَالِدِهِۦ شَيۡـًٔاۚ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞۖ
فَلَا تَغُرَّنَّكُمُ ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَا وَلَا يَغُرَّنَّكُم بِٱللَّهِ ٱلۡغَرُورُ ﴿٣٢﴾
إِنَّ ٱللَّهَ عِندَهُۥ عِلۡمُ ٱلسَّاعَةِ وَيُنَزِّلُ ٱلۡغَيۡثَ
وَيَعۡلَمُ مَا فِي ٱلۡأَرۡحَامِۖ وَمَا تَدۡرِي نَفۡسٞ مَّاذَا تَكۡسِبُ غَدٗاۖ
وَمَا تَدۡرِي نَفۡسُۢ بِأَيِّ أَرۡضٖ تَمُوتُۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌ خَبِيرُۢ ﴿٣٣﴾

ثمن

28. Shin baka sani ba (yakai abokin zance) haƙiƙa Allah (Tabaraka wa ta'ala) yana shigar da dare cikin wunin rana, yana shigar da wunin rana a cikin dare, (kowane daga ɗayaya karu da abinda ya tauwayi ɗayansa dashi,) kuma ya hore rana da wata, kowane (daga cikinsu) yana gudana a cikin falakinsa izuwa ajali abin ambato (shine ranar alƙiyama?) Haƙiƙa Ubangiji masanine karara da abinda kuke aikatawa.
29. Wannan abin ambato kuwa saboda Allah shine kaɗai tabbatacce, kuma abinda kuke bautawa ba Allah bashine banza kawai kuma haƙiƙa shine maɗaukaki (ga barin halittarsa da rinjaye) mai ƙasaitar girma.
30. Shin baka saniba cewa komaye tana gudana a cikin kogi da ni'imar Allah bane donya nuna muku (yaku abokan zance da wancananka) wani abu daga ayoyinsa (na girman Ubangiji?) Haƙiƙa akwai iznace-izinace ga dukkan haƙurau, (wato mai yawan haƙuri ga barin saɓon Allah) godiwa ga ni'imar Allah (wato mai yawan godiya a cikin wancananka).
31. Idan kumfa ta lullube kafirai kamar duwatsu (wacce take inuwance wanda yake ƙarƙashinta) saisu dinga kiran Allah suna masu tsarkake addu'a gareshi (donya tserar dasu, basa kiran kowa taredashi saishi.) To yayin daya tserar dasu izuwa gaci, to akwai daga cikinsu matsakaici (tsakanin kafirci da imani imani da wanda yake mai wanzuwa a kan kafircinsa,) barnai musu sai dukkan zambatau babban butulu ga ni'imomin Allah ta'ala.

(WA'AZI DASHIRYARWA)

32. Yaku waɗannan jama'a kuji tsoron Ubangijinku ku tsoraci rana wadda uba bazai magantawa ɓansa komai (a cikinta) wala abin haihuwa bazai magantawa ubansa komai ba (a cikinta,) haƙiƙa alƙawarin Ubangiji (da tashin alƙiyama) gaskiya ne, kada rayuwar duniya ta ruɗeku (ga barin aikin Musulunci,) kada shaiɗan ya ruɗekuda (haƙurin) Allah (da saurarawarsa).
33. Haƙiƙa Ubangiji sanin lokacin da alƙiyama zata tashi yana gurinsa, shine yake saukar da ruwa (a lokacindaza a yishi da gurindaza a yishi,) shine yasan abinda yake cikin mahaifai (namiji ko mace, bai sanar da kowa ɗayan wannan ukun basaishi (amma wannan bai hana yasanar da bayinsa da wani abu daga wannan ba, kamar Annabawa da Waliyyai. malamai sukace : "Allah bai fitarda Manzon Allah daga duniyaba, sai daya tsinkayar dashi bisa wancanankabiyar, saidai ya umarce shine da ɓoyeta (Sawi). Ba watakai data san abinda zatayi gobe (na hairi ko sharri-Allah ne yasani) ba watakai data san a yaushe zata mutu, (Allah ta'ala ne yasani,) haƙiƙa Ubangiji masanine da kowane abu, (masanine da zahirinsa kamar badininsa, Bukhari ya ruwaito ga Ibn Umara-Hadisin mafatihul gaibi biyar (5) ne.)

32 سُورَةُ السَّجْدَةِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ ثَلَاثُونَ ءَايَةً 30

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

الٓمٓ تَنزِيلُ الْكِتَٰبِ لَا رَيْبَ فِيهِ مِن رَّبِّ الْعَٰلَمِينَ (1) أَمْ يَقُولُونَ
افْتَرَىٰهُ بَلْ هُوَ الْحَقُّ مِن رَّبِّكَ لِتُنذِرَ قَوْمًا مَّا أَتَىٰهُم مِّن نَّذِيرٍ مِّن قَبْلِكَ
لَعَلَّهُمْ يَهْتَدُونَ (2) اللَّهُ الَّذِي خَلَقَ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا
فِي سِتَّةِ أَيَّامٍ ثُمَّ اسْتَوَىٰ عَلَى الْعَرْشِ مَا لَكُم مِّن دُونِهِ مِن وَلِيٍّ
وَلَا شَفِيعٍ أَفَلَا تَتَذَكَّرُونَ (3) يُدَبِّرُ الْأَمْرَ مِنَ السَّمَاءِ إِلَى الْأَرْضِ
ثُمَّ يَعْرُجُ إِلَيْهِ فِي يَوْمٍ كَانَ مِقْدَارُهُ أَلْفَ سَنَةٍ مِّمَّا تَعُدُّونَ (4)
ذَٰلِكَ عَٰلِمُ الْغَيْبِ وَالشَّهَٰدَةِ الْعَزِيزُ الرَّحِيمُ (5) الَّذِي أَحْسَنَ كُلَّ شَيْءٍ خَلَقَهُ
وَبَدَأَ خَلْقَ الْإِنسَٰنِ مِن طِينٍ (6) ثُمَّ جَعَلَ نَسْلَهُ مِن سُلَٰلَةٍ
مِّن مَّاءٍ مَّهِينٍ (7) ثُمَّ سَوَّىٰهُ وَنَفَخَ فِيهِ مِن رُّوحِهِ وَجَعَلَ لَكُمُ السَّمْعَ وَالْأَبْصَٰرَ
وَالْأَفْئِدَةَ قَلِيلًا مَّا تَشْكُرُونَ (8) وَقَالُوا أَ۬ذَا ضَلَلْنَا فِي الْأَرْضِ
ربع
إِنَّا لَفِي خَلْقٍ جَدِيدٍ (9) بَلْ هُم بِلِقَاءِ رَبِّهِمْ كَٰفِرُونَ (10) * قُلْ يَتَوَفَّىٰكُم
مَّلَكُ الْمَوْتِ الَّذِي وُكِّلَ بِكُمْ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُمْ تُرْجَعُونَ (11)

Suratus Sajadati

A Makka Aka. Saukar Da Ita Ayoyinta Talatin (30)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

ABINDA YAKE CIKIN WANNAN SURA YA ƘUNSHI KIRARI GA ƘUR'ANI DA MANA KANSA DA GIRMAN MUTUM. MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA YANA KARANTA WANNAN SURA A SALLAR ALFIJIR DA HAL-ATE-ALAL-INSANI, KUMA AN RUWAITO MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA YANA KARANTA SURATU SAJADATI DA TABARAKA) (KIRARIN ALƘUR'ANI GA ALLAH)

1.A.L.M. (Allahu a'a-lamu-bi-muradihi-bi-zalika.) Saukarwar Alƙur'ani ba kokonto a cikinsa, daga Ubangijin talikai.

2. Kai bari! suna cewa Annabi Sallallahu alaihi wasallama ƙirƙirarsa yayi. A'a, bari! Shine tabbas daga Ubangijinka donka tsoratar da mutane waɗanda gargaɗi baizo musu ba gabanka, ana ƙaunarsu shiriya (da gargaɗinka).

3. Allah Shine Sarkin daya halicci sammai da ƙassaida abinda yake tsakaninsu a cikin kwanaki shida, (farkonsu ranar Lahadi, ƙarshensu ranar Juma'a) sannan yayi daidai a kan gadon mulki (daidaituwa data dace dashi. Bakuda wani majibinci (yaku kafiran Makka) ba Allah ba wala mai ceto (dazai ije azabarsa ga buranku) shin bakwa tuna (wannan ku bada gaskiya) ba?

4. Yana shirya lamari daga sama izuwa ƙasa (muddar duniya,) sannan (lamari) yakoma izuwa gareshi (da dukkan shirye-shirye) a cikin rana wadda gwargwadonta shekara dubu daga abinda kuke ƙirgawa (a duniya a cikin Suratu Sa'ala shekara dubu hamsin, shine ranar alƙiyama saboda tsananin tsarmakatanta dangane da kafiri amma mumini saiya zama mafi sauƙi gareshi daga sallar farilla da yake sallatarta a duniya, tamfar yadda yazo cikin Hadisi).

5. Wancananka (mahalicci mai shirye shirye) Shine masanin asirin fake da abinda yake a bayyane, mabuwayi (a cikin mulkinsa,) mai jinƙai (ga mutanen ɗa'arsa).

6. Wanda ya kyautata kowane abu daya halicce shi, yafara halittar Annabi Adamu (alaihissalamu) daga yumɓu.

7. Sannan ya halicci zuriyyarsa daga gudan jini daga ruwa wulaƙantacce (shine digon maniyyi).

8. Sannan ya daidaita halittar Annabi (Adamu alaihissalamu) ya busa a cikinsa dagarai dake cikin mulkinsa (ai Ya sanyashi rayayye mai hasashe, bayan ya kasance sandararre) yasanya kunnuwa gareku (ku zuriyar Annabi Adamu alaihissalamu) da idanduna da zukata, kaɗan kwarai kuke godewa (Allah).

(MUSUNSU DA TASHIN ALƘIYAMA)

9. Masu musun alƙiyama sukace, Yanzu idan mun ɓata a cikin ƙasa (shine muka zama turɓaya, muna cudanye da turɓayar ƙasa) shin mu muna cikin halitta sabuwa?

10. Bari! Su masu kafircewa ne da tashin alƙiyama.

11. Cene (dasu) "Mala'ikan mutuwa zai karɓi ranku wanda aka wakkala da karɓar rayukanku, sannan izuwa Ubangijin zaku koma (yayi muku sakamako da ayyukanku).

وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذِ ٱلْمُجْرِمُونَ نَاكِسُوا۟ رُءُوسِهِمْ عِندَ رَبِّهِمْ
رَبَّنَآ أَبْصَرْنَا وَسَمِعْنَا فَٱرْجِعْنَا نَعْمَلْ صَٰلِحًا إِنَّا مُوقِنُونَ ﴿12﴾
وَلَوْ شِئْنَا لَءَاتَيْنَا كُلَّ نَفْسٍ هُدَىٰهَا وَلَٰكِنْ حَقَّ ٱلْقَوْلُ
مِنِّى لَأَمْلَأَنَّ جَهَنَّمَ مِنَ ٱلْجِنَّةِ وَٱلنَّاسِ أَجْمَعِينَ ﴿13﴾ فَذُوقُوا۟
بِمَا نَسِيتُمْ لِقَآءَ يَوْمِكُمْ هَٰذَآ إِنَّا نَسِينَٰكُمْ وَذُوقُوا۟
عَذَابَ ٱلْخُلْدِ بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿14﴾ إِنَّمَا يُؤْمِنُ بِـَٔايَٰتِنَا
ٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِّرُوا۟ بِهَا خَرُّوا۟ سُجَّدًا وَسَبَّحُوا۟ بِحَمْدِ رَبِّهِمْ
وَهُمْ لَا يَسْتَكْبِرُونَ ۩ ﴿15﴾ تَتَجَافَىٰ جُنُوبُهُمْ عَنِ ٱلْمَضَاجِعِ يَدْعُونَ
رَبَّهُمْ خَوْفًا وَطَمَعًا وَمِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ يُنفِقُونَ ﴿16﴾
فَلَا تَعْلَمُ نَفْسٌ مَّآ أُخْفِىَ لَهُم مِّن قُرَّةِ أَعْيُنٍ جَزَآءًۢ بِمَا كَانُوا۟
يَعْمَلُونَ ﴿17﴾ أَفَمَن كَانَ مُؤْمِنًا كَمَن كَانَ فَاسِقًا ۚ لَّا يَسْتَوُۥنَ ﴿18﴾
أَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَلَهُمْ جَنَّٰتُ ٱلْمَأْوَىٰ
نُزُلًۢا بِمَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿19﴾ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ فَسَقُوا۟
فَمَأْوَىٰهُمُ ٱلنَّارُ ۖ كُلَّمَآ أَرَادُوٓا۟ أَن يَخْرُجُوا۟ مِنْهَآ أُعِيدُوا۟ فِيهَا
وَقِيلَ لَهُمْ ذُوقُوا۟ عَذَابَ ٱلنَّارِ ٱلَّذِى كُنتُم بِهِۦ تُكَذِّبُونَ ﴿20﴾

سجدة

12. Da kana ganin zamanin da kafirai suke masu sunkuyar da kayukansu nan ga Ubangijinsu (saboda kunya) suna cewa Ya Ubangijinmu, munga (abinda muka musa na tashin alƙiyama) munji (mun gasgata manzanni daga gareka cikin abinda muka ƙaryatasu daga gareka) to, komar damu izuwa duniya mu aikata aiki nagari (a cikinta,) haƙiƙa mu masu sakankancewa ne (a yanzu, to wannan bazai amfanesu ba, bakuma zasu koma duniya ba, dakaga al'amari mai firgitarwa).

13. Da Munga dama da Mun baiwa kowace kai shiriyarta (tashiriya da imani da ɗa'a da zaɓi daga gareta,) saidai magana dai gareni ta tabbatashine Wallahi zan cika jahannama da aljanu da mutane baki ɗaya.

14. To ku ɗanɗani azabasaboda mantuwar gamuwarkuda wannan rana, (don kun bar bada gaskiya dashi) haƙiƙa Munbar ku a cikin wannan azabaku ɗanɗani azabar dauwama saboda abinda kuke aikatawa (na kafirci da ƙaryatawar manzanni).

(WAƊANNAN SUNE MUMINAI, WANNAN SHINE SAKAMAKONSU)

15. Dahir waɗanda suke bada gaskiya da ayoyinmu (Alƙur'ani) sune waɗanda idan aka gargaɗesu da ita sukan faɗi suna masu dungura goshinsu suna tsarkakewa da godiyar Ubangijinsu Su basa girmankai (saburan imani da ɗa'a).

16. Haƙurƙuransu tana nisantar shinfiɗarsu suna salla ta ƙiyamul-Laili) suna tsoro daga azabar Ubangiji da kawazuci ga rahamarsa suna ciyarwa daga abinda Muka azurta musu (sadaka da kyauta).

17. Ba watakai data san abinda aka ɓoye musu nadaga sanyin idaniya don sakamako daga abinda suka kasance suna aikatawa.

18. Shin wanda ya kasance mumini zai zama kamar wanda ya kasance fasiƙi? Bazasuyi daidai ba.

19. Amma waɗanda suka bada gaskiya suka aikata ayyuka nagargaru, to aljannar makoma na garesu don garar baƙi saboda abinda suke aikatawa.

20. Amma waɗanda sukayi fasiƙanci (da kafirci da karyatawa) to makomar su wuTace duk zamanin da suka nemi su fita daga cikinta, sai a mayar dasu cikinta a ce dasu "Ku ɗanɗani azabar wuta wadda kuka kasance kuna ƙaryatawa da ita."

وَلَنُذِيقَنَّهُم مِّنَ ٱلْعَذَابِ ٱلْأَدْنَىٰ دُونَ ٱلْعَذَابِ ٱلْأَكْبَرِ
لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿21﴾ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن ذُكِّرَ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِۦ
ثُمَّ أَعْرَضَ عَنْهَآ إِنَّا مِنَ ٱلْمُجْرِمِينَ مُنتَقِمُونَ ﴿22﴾
۞ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَى ٱلْكِتَٰبَ فَلَا تَكُن فِى مِرْيَةٍ مِّن لِّقَآئِهِۦ ثمن
وَجَعَلْنَٰهُ هُدًى لِّبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ﴿23﴾ وَجَعَلْنَا مِنْهُمْ أَئِمَّةً
يَهْدُونَ بِأَمْرِنَا لَمَّا صَبَرُوا۟ ۖ وَكَانُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا يُوقِنُونَ ﴿24﴾
إِنَّ رَبَّكَ هُوَ يَفْصِلُ بَيْنَهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ فِيمَا
كَانُوا۟ فِيهِ يَخْتَلِفُونَ ﴿25﴾ أَوَلَمْ يَهْدِ لَهُمْ
كَمْ أَهْلَكْنَا مِن قَبْلِهِم مِّنَ ٱلْقُرُونِ يَمْشُونَ فِى مَسَٰكِنِهِمْ ۚ
إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَٰتٍ ۖ أَفَلَا يَسْمَعُونَ ﴿26﴾
أَوَلَمْ يَرَوْا۟ أَنَّا نَسُوقُ ٱلْمَآءَ إِلَى ٱلْأَرْضِ ٱلْجُرُزِ
فَنُخْرِجُ بِهِۦ زَرْعًا تَأْكُلُ مِنْهُ أَنْعَٰمُهُمْ وَأَنفُسُهُمْ ۖ
أَفَلَا يُبْصِرُونَ ﴿27﴾ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلْفَتْحُ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿28﴾
قُلْ يَوْمَ ٱلْفَتْحِ لَا يَنفَعُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ إِيمَٰنُهُمْ
وَلَا هُمْ يُنظَرُونَ ﴿29﴾ فَأَعْرِضْ عَنْهُمْ وَٱنتَظِرْ إِنَّهُم مُّنتَظِرُونَ ﴿30﴾

21. Lalle zamu ɗanɗana musu azaba mafi kusanci (azabar duniya da kisa da ribacewa da fari mai daɗewa da cutuka,) kuma bayan azaba mafi girma (azabar Lahira) ana saransa komo izuwa imani.
22. Waye mafi zalinci daga wanda aka gargaɗeshi da ayoyin Ubangijinsa sanna ya bujire ga buranta? (Ba mafi zalince daga gareshi) to haƙiƙa Mu masuyin azabane ga kafirai.

(GARGADE-GARGADE DA IZNACE-IZNACE)

23. Haƙiƙa Mun baiwa Annabi Musa (alaihissalamu) Attaura kada kazamo cikin kokonto cikin saduwa dashi (haƙiƙa sun sadu a daren Isra'i,) Mun sanya Annabi Musa shiriyaga Bani-Isra'ila.
24. Mun sanyashiwagabanni daga garesu dasuke shiryar da (mutane) da umarninmu yayin da suka ɗaure (kan addininsu kuma suka daure kan bala'o'i na daga magautansu,) sun kasance suna sakankancewa da ayoyinmu.
25. Haƙiƙa Ubangijinka Shine mai rarrabe (hukunci) tsakaninsu ranar Alƙiyama cikin abinda suka kasance suna saɓawa a cikinsa (na lamarin addini).
26. Shin bai bayyana garesu ba nawa Muka halakar gabansu na al'umma na daga tsareku saboda kafircinsu, suna tafiya guraren zamansu cikin Sham da wanin-ta, to suyi izna mana). Haƙiƙa akwai ayoyi cikin wancananka, shin basa jin Alƙur'anine jin karɓa?
27. Shin basu ganibane cewa Mu Muna kora ruwa izuwa ƙasa ƙeƙashashshiya (wacce ba tsiri cikinta wacce ba ruwa,) Muka fitar da hatsi da ruwannan, da dabbobinsu zasu ci daga cikinsa da kawukansu, shin basu ga (wannan basu san cewa Mu masu ikone a kan Mu mayar dasu bayan sun mutu).
28. Suna cewa (da muminai) "Yaushe ne wannan hukunci inkun kasance magasgata?"
29. Cene (dasu) "Hukunci da saukar azaba garesu waɗanda suka kafirtada Allah imaninsu bazai amfane su da komai ba, baza ayi musu sauraro su tuba ba, ko suyi hanzari.
30. To rabu dasu ka saurari saukar azaba garesu, haƙiƙa su masu aren mutuwarka ne (ko kasheka donsu huta daga gareka, to wannan gaban umarnine da kashesu).

33 سُورَةُ الأحزاب مدنية
وهي ثلاث وسبعون آية 73

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيٓءُ ٱتَّقِ ٱللَّهَ وَلَا تُطِعِ ٱلْكَٰفِرِينَ وَٱلْمُنَٰفِقِينَ
إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا حَكِيمًا ﴿1﴾ وَٱتَّبِعْ مَا يُوحَىٰٓ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ
إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرًا ﴿2﴾ وَتَوَكَّلْ عَلَى ٱللَّهِ
وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلًا ﴿3﴾ مَّا جَعَلَ ٱللَّهُ لِرَجُلٍ مِّن قَلْبَيْنِ فِي جَوْفِهِۦ
وَمَا جَعَلَ أَزْوَٰجَكُمُ ٱلَّٰٓـِٔي تَظَّهَّرُونَ مِنْهُنَّ أُمَّهَٰتِكُمْ وَمَا جَعَلَ أَدْعِيَآءَكُمْ
أَبْنَآءَكُمْ ذَٰلِكُمْ قَوْلُكُم بِأَفْوَٰهِكُمْ وَٱللَّهُ يَقُولُ ٱلْحَقَّ وَهْوَ يَهْدِي ٱلسَّبِيلَ ﴿4﴾
ٱدْعُوهُمْ لِءَابَآئِهِمْ هُوَ أَقْسَطُ عِندَ ٱللَّهِ فَإِن لَّمْ تَعْلَمُوٓاْ ءَابَآءَهُمْ
فَإِخْوَٰنُكُمْ فِي ٱلدِّينِ وَمَوَٰلِيكُمْ وَلَيْسَ عَلَيْكُمْ جُنَاحٌ فِيمَآ أَخْطَأْتُم بِهِۦ
وَلَٰكِن مَّا تَعَمَّدَتْ قُلُوبُكُمْ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿5﴾
* ٱلنَّبِيٓءُ أَوْلَىٰ بِٱلْمُؤْمِنِينَ مِنْ أَنفُسِهِمْ وَأَزْوَٰجُهُۥٓ أُمَّهَٰتُهُمْ وَأُوْلُواْ ٱلْأَرْحَامِ
بَعْضُهُمْ أَوْلَىٰ بِبَعْضٍ فِي كِتَٰبِ ٱللَّهِ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُهَٰجِرِينَ إِلَّآ أَن
تَفْعَلُوٓاْ إِلَىٰٓ أَوْلِيَآئِكُم مَّعْرُوفًا كَانَ ذَٰلِكَ فِي ٱلْكِتَٰبِ مَسْطُورًا ﴿6﴾

ربع

Suratul Ahzabi

A Madina Aka. Saukar Da Ita Ayoyinta Saba'in.Da Uku (73)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

(WANNAN SURA TA ƘUNSHI KUN-YATAR MUNAFUKAI, DA SUKAN DA SUKAYI CIKIN AURENSA GA MATAYENSA, DA MATSAYIN MU-NAFUKAI A GAZWATIL-AHZABI, DA WANINTA, DA BAYANIN ANNABCI, DA ƘISSAR ZAIDU DAN HARISATA, DAYABON MA'AIKIN ALLAH, DA SAHABBANSA, DA LADUBBANA MUSULUNCI) (FUSKANCE-FUSKANCE GA LADUBBA)

1. Ya wannan Annabi; dauwamu bisa tsoron Allah kada kabi kafirai da munafukai (a cikin abinda ya saɓi shari'arka,) haƙiƙa Ubangiji ya tabbata masani (da abindazai kasance tun gaban kasancewarsa) gwani (cikin halittarsa).
2. Kabi abinda ake aikowa izuwa gareka daga Ubangijinka, lalle Ubangiji ya tabbata cikakken masani da abinda suke aikatawa.
3. Ka dogara bisa Ubangiji (a cikin lamarinka,) Ubangiji ya isa mai kiyayeka, (al'umma tasa mabiya ne gareka a cikin wancananka dukansa).

(RADDIN UBANGIJI TA'ALA GA MAI KATOBARA MAI IZGILI GA ANNABI (SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA) DA LADAFTARWA GA SAHABBAN ANNABI (SALLALLAHU ALAIHI WASALLANA) A CIKIN DANGANA ƊA GA ANNABI (SAL-LALLAHU ALAIHI WASALLAMA) WATO ZAIDU). DAN HARISATA

4. Allah Ubangiji bai sanya zuciya biyu a cikin mutum ba, (raddi ne bisa wanda ya faɗa daga kafirai cewa yana da zuciya biyu a cikin cikinsa, yana hankalta daga kowacce fiyeda abinda Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) yake hankalta,) Allah bai sanya matayenku waɗanda kuke bayantasu (kamar mutum yace da matarsa ke a gareni kamar bayan mahaifiya ta kike Shine bayantawa,) bai sanya su iyayenku ba, (ai kamar iyayenku a cikin haramtawa saboda a Jahiliyya ana ƙirga wannan shika kamar yadda aka faɗa a Suratul-Mujadatai, kaffara ce kaɗai ga wannan, ga sharadinsa kamar yadda aka faɗa a Suratul Mujadilati,) bai sanya 'ya'yanku na rana ba 'ya'yayenku na haƙiƙa, wancananku maganarku ce ga bakunanku (yaku Yahudu da munafukai, sun faɗi haka ga zainabu yar jahshu wacce Zaidu ɗan Harisata ya sake tashi kuma Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) ya aureta sai sukace Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) ya auri matar ɗansa, sai Allah ya ƙaryata su, Ubangiji yana fadar gaskiYakuma Shine mai shiryarwa izuwa hanyar gaskiya.
5. Ku kirasu izuwa iyayensu Shine mafi adalci nan ga Allah, inbaku san iyayensu ba to 'yan uwankune cikin addini kuma 'ya'yan amminku ne, babu laifi gareku cikin abinda kuka kuskure dashi cikin wancananka, saidai abinda zukatanku ta ganganta, (Shine bayanin hani,) Ubangiji ya tabbata mai gafara (da abinda ya kasance tun gaban hani,) mai jinkai ne (cikin wancananka).

(MATSAYIN MA'AIKIN ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA DANGANE DA MUMINAI TAREDA DAUKAKAR DARAJA A KANSU KUMA CEWA ANNABI (SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA) SHINE MAFI GIRMAN WASIDAR NI'IMA DATA SAMU IZUWA HALITTada HA-RAMCIN MATAYENSA GA DUKKAN MUSULMI, DA SHAFE GADO DA HIJIRA DA IMANI SHAFE SHIDA MAZOWA MAHAIFA)

6. Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) Shine mafi cancanta ga muminai daga kawukansu (a cikin abinda ya kirawo izuwa gareshi kuma kawukansu suka kirasu izuwa saɓaninsa,) matayensa iyayensune a (cikin haramcin aurensu a garesu,) ma'abota zumunce-zumunce, sashinsu mafi cancanta ne (a cikin gado) daga sashi a cikin littafin Allah, na muminai da muhajirai, (wato na gado da imani da hijira, wanda ya kasance a farkon Musulunci aka =

وَإِذْ أَخَذْنَا مِنَ النَّبِيِّـۧنَ مِيثَاقَهُمْ وَمِنكَ وَمِن نُّوحٍ وَإِبْرَٰهِيمَ
وَمُوسَىٰ وَعِيسَى ابْنِ مَرْيَمَ وَأَخَذْنَا مِنْهُم مِّيثَاقًا غَلِيظًا ﴿٧﴾
لِّيَسْـَٔلَ الصَّـٰدِقِينَ عَن صِدْقِهِمْ وَأَعَدَّ لِلْكَـٰفِرِينَ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿٨﴾
يَـٰٓأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُوا اذْكُرُوا نِعْمَةَ اللَّهِ عَلَيْكُمْ
إِذْ جَآءَتْكُمْ جُنُودٌ فَأَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ رِيحًا وَجُنُودًا لَّمْ تَرَوْهَا
وَكَانَ اللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرًا ﴿٩﴾ إِذْ جَآءُوكُم
مِّن فَوْقِكُمْ وَمِنْ أَسْفَلَ مِنكُمْ وَإِذْ زَاغَتِ الْأَبْصَـٰرُ
وَبَلَغَتِ الْقُلُوبُ الْحَنَاجِرَ وَتَظُنُّونَ بِاللَّهِ الظُّنُونَا ﴿١٠﴾
هُنَالِكَ ابْتُلِىَ الْمُؤْمِنُونَ وَزُلْزِلُوا زِلْزَالًا شَدِيدًا ﴿١١﴾ وَإِذْ يَقُولُ
الْمُنَـٰفِقُونَ وَالَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ مَّا وَعَدَنَا اللَّهُ وَرَسُولُهُۥٓ إِلَّا غُرُورًا ﴿١٢﴾
* وَإِذْ قَالَت طَّآئِفَةٌ مِّنْهُمْ يَـٰٓأَهْلَ يَثْرِبَ لَا مُقَامَ لَكُمْ فَارْجِعُوا ثمن
وَيَسْتَـْٔذِنُ فَرِيقٌ مِّنْهُمُ النَّبِىَّ يَقُولُونَ إِنَّ
بُيُوتَنَا عَوْرَةٌ وَمَا هِىَ بِعَوْرَةٍ إِن يُرِيدُونَ إِلَّا فِرَارًا ﴿١٣﴾
وَلَوْ دُخِلَتْ عَلَيْهِم مِّنْ أَقْطَارِهَا ثُمَّ سُئِلُوا
الْفِتْنَةَ لَـَٔاتَوْهَا وَمَا تَلَبَّثُوا بِهَآ إِلَّا يَسِيرًا ﴿١٤﴾

shafe shi) saidai koku aikata abin alheri izuwa waliyyanku (dayin wasiyya, to wannan ya halatta,) wancananka (shafe gado da imani da hijira, da gadarwa mazowa mahaifa) ya kasance abin rubutawa a Littafi (na LAUHUL MAHFUZU, ana nufin da Kitabullahi dayagabatada al-Kitabu na yanzu LAUHUL MAHFUZU).

(DAUKAKAR MARTABAR MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA BISA DUKKAN MA'AIKA)

7. Ka ambata zamanin da Muka karɓi alƙawarin Annabawa daga garesu (zamanin da aka fitar dasu daga tsatson Annabi Adamu alaihissalamu kamar kiyashi, kuma Muka riƙa daga gareka kuma daga Annabi Nuhu da Annabi Ibrahimu da Annabi Musa da Annabi Isa Dan maryamu, (Tsira da amincin Allah su tabbata garesu, wato su bautawa Allah suyi kira izuwa bauta tasa, Muka riƙi alƙawari kakƙaura daga garesu.
8. Don Ubangiji ya tambayi magasgata ga gaskiyarsu (a cikin isarda aike don gasgatawa wato munanawa ga kafirai gasu Annabawa,) Ubangiji ya tanadaji azaba mai raɗaɗi ga kafirai (masu ƙaryata Annabawa).

(YAƘIN GWALALO KO LAHZABU WATO RUNDUNA)

9. Yaku waɗanda suka bada gaskiYaku ambaci ni'imar Ubangiji gareku yayin da runduna sukazo muku (na kafirai, sunyi kungiya kwanukan hakan gwalalo) Muka aika da iska garesu da runduna wacce baku ganta ba (ta Mala'iku) Ubangiji mai ganine da abinda kuke aikatawa Shine hakan gwalalo da tattarar tawagar kafirai.
10. Zamanin da sukazo muku ta burbushinku data ƙarƙashinku na gabas dayamma, dayayin da idanduna suka karkace ga buran komai izuwa magautanta ta kowane gefe, zukata suka iso matuƙar maƙogwaro (saboda tsananin tsoro) kuna yin mummunan zatutuwa (ga Allah, mai sassaɓawa da taimako da ɗebe haso).
11. Cananka ne aka jarrabi muminai (don mai ikhlasi ya bayyana daga waninsa,) aka girgizasu girgizawa mai tsanani (saboda tsananin firgita).
12. To ka ambata zamanin da munafukai suke cewa da waɗanda raunin ƙuduri yake zukatansu "Allah da ma'aikinsa basuyi mana alƙawarin komai basai ruɗi,
13. Kuma zamanin waɗansu yanki daga cikinsu sukace "Yaku mutanen Madina ba martaba gareku ko gurin zama, ku koma (izuwa gidaddajinku na Madina, sun kasance sun fito tareda Annabi Sallallahu alaihi wasallama izuwa dutsen Sal'u dutse ne daga wajen Madina sun fito saboda yaƙi,) waɗansu mutane daga cikinsu suna neman izinin ma'aikin Allah (Sallallahu alaihi wasallama a cikin komawa gidasuna cewa gidaddajinmu tsirara suke (bakatangaggu ne ba munajin tsoro a gareta, Ubangiji yace;) "Alhali ita ba tsirara take ba, basa nufin komai sai gudu (daga yaƙi)".
14. Da an shigo Madina a kansu daga sassanta sannan masu shigowa su tambayi fitina wato shirka, dasun zo mata sun aikatata bazasu zauna a Madina basai kaɗan.

وَلَقَدْ كَانُواْ عَاهَدُواْ اللَّهَ مِن قَبْلُ لَا يُوَلُّونَ الْأَدْبَارَ
وَكَانَ عَهْدُ اللَّهِ مَسْـُٔولًا ﴿15﴾ قُل لَّن يَنفَعَكُمُ الْفِرَارُ
إِن فَرَرْتُم مِّنَ الْمَوْتِ أَوِ الْقَتْلِ وَإِذًا لَّا تُمَتَّعُونَ
إِلَّا قَلِيلًا ﴿16﴾ قُلْ مَن ذَا الَّذِي يَعْصِمُكُم مِّنَ اللَّهِ
إِنْ أَرَادَ بِكُمْ سُوٓءًا أَوْ أَرَادَ بِكُمْ رَحْمَةً
وَلَا يَجِدُونَ لَهُم مِّن دُونِ اللَّهِ وَلِيًّا
وَلَا نَصِيرًا ﴿17﴾ قَدْ يَعْلَمُ اللَّهُ الْمُعَوِّقِينَ مِنكُمْ
وَالْقَآئِلِينَ لِإِخْوَانِهِمْ هَلُمَّ إِلَيْنَا وَلَا يَأْتُونَ الْبَأْسَ
إِلَّا قَلِيلًا ﴿18﴾ أَشِحَّةً عَلَيْكُمْ فَإِذَا جَآءَ الْخَوْفُ
رَأَيْتَهُمْ يَنظُرُونَ إِلَيْكَ تَدُورُ أَعْيُنُهُمْ كَالَّذِي يُغْشَىٰ عَلَيْهِ
مِنَ الْمَوْتِ فَإِذَا ذَهَبَ الْخَوْفُ سَلَقُوكُم بِأَلْسِنَةٍ حِدَادٍ
أَشِحَّةً عَلَى الْخَيْرِ أُوْلَٰٓئِكَ لَمْ يُؤْمِنُواْ فَأَحْبَطَ اللَّهُ أَعْمَالَهُمْ
وَكَانَ ذَٰلِكَ عَلَى اللَّهِ يَسِيرًا ﴿19﴾ ۞ يَحْسَبُونَ الْأَحْزَابَ لَمْ يَذْهَبُواْ
وَإِن يَأْتِ الْأَحْزَابُ يَوَدُّواْ لَوْ أَنَّهُم بَادُونَ فِي الْأَعْرَابِ
يَسْـَٔلُونَ عَنْ أَنۢبَآئِكُمْ وَلَوْ كَانُواْ فِيكُم مَّا قَاتَلُوٓاْ إِلَّا قَلِيلًا ﴿20﴾

رُبع

15. Lalle sunyi alƙawari tun gaba bazasu juya ba, alƙawarin Allah ya tabbata abin tambayo ga barin cikawa dashi.
16. Cene "Gudu bazai amfane ku daga mutuwa ko kisa, yayin nan inkun gudu baza a jiyar daku daɗi a duniya ba, bayan gudunku sai kaɗan (gwargwadon ajalinku).
17. Cene, "Su waye waɗannan dasuke kiyaye ku daga Allah in yayi nufin mummuna daku, ko yayi nufin alheri daku? Basuda wani majibinciin ba Allah ba, wala mai ijewar wuta ga buransu, wala mai taimako.
18. Haƙiƙa Ubangiji ya an masu sanyaya gwiwa daga cikinkuda masu cewa da 'yan uwansu kuzo izuwa garemu, basa halartar yaƙi sai kaɗan (don riya da jiyarwa).
19. Masu kwauron taimako a gareku (wato basa taimakonku) idan tsoro yazo saika gansu suna duba izuwa gareka idandunansu na kewayawa, kamar kewayawar wanda ake suma gareshi saboda magagin mutuwa, idan tsoro yakau (aka kwashi ganima,) saisu cucekuda harasa kaifafa masu kwauro kan alheri, (wato ganima dasuke neman ta,) wadancannanka basu bada gaskiyaba a haƙiƙa, saboda haka Allah ya lalata ayyukansu, lalata aiki ya kasance mai sau□ine ga Allah.
20. Suna zaton ƙungiyar kafirai basu tafi izuwa Makka ba saboda tsoronsu daga garesu, idan ƙungiyar kafiran nan suka sake komowa izuwa garesu, zasu guraci cewa dama sunacan a ƙauye a cikin Larabawan ƙauye suna tambayo ga labarinku tareda kafirai, dasun kasance a cikinku a wannan yayin baza suyi yaƙi basai kaɗan don riya da tsoron laifantawa.

لَقَدْ كَانَ لَكُمْ فِي رَسُولِ اللَّهِ إِسْوَةٌ حَسَنَةٌ
لِّمَن كَانَ يَرْجُوا اللَّهَ وَالْيَوْمَ الْآخِرَ وَذَكَرَ
اللَّهَ كَثِيرًا ﴿21﴾ وَلَمَّا رَءَا الْمُؤْمِنُونَ الْأَحْزَابَ قَالُوا
هَٰذَا مَا وَعَدَنَا اللَّهُ وَرَسُولُهُۥ وَصَدَقَ اللَّهُ وَرَسُولُهُۥ
وَمَا زَادَهُمْ إِلَّا إِيمَانًا وَتَسْلِيمًا ﴿22﴾ مِّنَ الْمُؤْمِنِينَ رِجَالٌ
صَدَقُوا مَا عَاهَدُوا اللَّهَ عَلَيْهِ فَمِنْهُم مَّن قَضَىٰ نَحْبَهُۥ
وَمِنْهُم مَّن يَنتَظِرُ وَمَا بَدَّلُوا تَبْدِيلًا ﴿23﴾
لِّيَجْزِيَ اللَّهُ الصَّٰدِقِينَ بِصِدْقِهِمْ وَيُعَذِّبَ الْمُنَٰفِقِينَ إِن شَا
أَوْ يَتُوبَ عَلَيْهِمْ إِنَّ اللَّهَ كَانَ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿24﴾
وَرَدَّ اللَّهُ الَّذِينَ كَفَرُوا بِغَيْظِهِمْ لَمْ يَنَالُوا خَيْرًا
وَكَفَى اللَّهُ الْمُؤْمِنِينَ الْقِتَالَ وَكَانَ اللَّهُ قَوِيًّا عَزِيزًا ﴿25﴾
وَأَنزَلَ الَّذِينَ ظَٰهَرُوهُم مِّنْ أَهْلِ الْكِتَٰبِ مِن
صَيَاصِيهِمْ وَقَذَفَ فِي قُلُوبِهِمُ الرُّعْبَ فَرِيقًا تَقْتُلُونَ
وَتَأْسِرُونَ فَرِيقًا ﴿26﴾ وَأَوْرَثَكُمْ أَرْضَهُمْ وَدِيَٰرَهُمْ وَأَمْوَٰلَهُمْ وَأَرْضًا
لَّمْ تَطَـُٔوهَا وَكَانَ اللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرًا ﴿27﴾

(ƘANƘAME SUNNAR ANNABI RASULULLAHI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

21. Haƙiƙa koyi kyakkyawa ya kasance gareku a cikin Ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wasallama, a cikin yaƙi da tabbata a gurin tabbata ga wanda yake tsoron Allah ya ambaci Allah ambato maiyawa saɓanin wanda bai kasance haka ba.
22. Yayin da muminai sukaga rundunar kafirai sai sukace, wannan Shine abinda Allah yayi mana alƙawari da manzonsa Sallallahu alaihi wasallama na daga jarrabada taimako. Allah da ma'aikinsa sun gasgata cikin alƙawari, wannan bai ƙara musu komai ba sai imani wato gasgatawa da imani da miƙa wuyaga al'amarinsa.
23. Akwai daga muminai mazaje da suka gasgata abinda suka yiwa Allah alƙawari a kansa na tabbata tareda ma'aikin Allah sallallahu alaiht wasallama, akwai daga cikinsu wanda ya biya buƙatarsa Shine ya mutu ko a kasheshi fisabililLahi, akwai daga cikinsu wanda yake sauraron wannan, basu musanya a cikin alƙawari saɓanin munafukai ba, Allah yayi haka,
24. Saboda yasakawa masu gaskiya da gaskiyarsu ya azabci munafukai in yaga dama Shine ya matar dasu a kan munafuncinsu koya karɓi tubansu, Ubangiji mai gafarne ga wanda a tuba mai jinƙai ne dashi.
25. Ubangiji ya mayar da waɗanda suka kafirta daga rundunar kafirai da fushinsu basu sami muradinsu bana daga rinjaye daga muminai, Ubangiji ya hutar da muminai yaƙi da iska da Mala'iku, Ubangiji mai ƙarfine bisa samar da abinda yake nufi, mai rinjaye ne bisa lamarinsa.
26. Ya saukar da waɗanda suka taimake su daga mazowa littafi sune ƙuraizatu daga manyan biranensu, ya jefa firgita a zukatansu kuna kashe wata jama'a daga cikinsu, sune waɗanda sukayi yaƙi kuna ribace wata daga cikinsu sune zuriyyarsu.
27. Yagadar daku ƙasarsu da gidaddajinsu da dukiyoyinsu da ƙasa wacce baku taɓa takata ba bayan nan, Itace Haibara da watanta izuwa ranar alƙiyama, an karɓi Haibaru bayan ƙuraizatu. Ubangiji mai ikone bisa komai.

ثمن

۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ قُل لِّأَزْوَٰجِكَ إِن كُنتُنَّ تُرِدْنَ ٱلْحَيَوٰةَ
ٱلدُّنْيَا وَزِينَتَهَا فَتَعَالَيْنَ أُمَتِّعْكُنَّ وَأُسَرِّحْكُنَّ سَرَاحًا جَمِيلًا ﴿28﴾
وَإِن كُنتُنَّ تُرِدْنَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَٱلدَّارَ ٱلْـَٔاخِرَةَ
فَإِنَّ ٱللَّهَ أَعَدَّ لِلْمُحْسِنَٰتِ مِنكُنَّ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿29﴾
يَٰنِسَآءَ ٱلنَّبِيِّ مَن يَأْتِ مِنكُنَّ بِفَٰحِشَةٍ مُّبَيِّنَةٍ
يُضَٰعَفْ لَهَا ٱلْعَذَابُ ضِعْفَيْنِ وَكَانَ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرًا ﴿30﴾
وَمَن يَقْنُتْ مِنكُنَّ لِلَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَتَعْمَلْ صَٰلِحًا
نُّؤْتِهَآ أَجْرَهَا مَرَّتَيْنِ وَأَعْتَدْنَا لَهَا رِزْقًا كَرِيمًا ﴿31﴾
يَٰنِسَآءَ ٱلنَّبِيِّ لَسْتُنَّ كَأَحَدٍ مِّنَ ٱلنِّسَآءِ إِنِ ٱتَّقَيْتُنَّ
فَلَا تَخْضَعْنَ بِٱلْقَوْلِ فَيَطْمَعَ ٱلَّذِى فِى قَلْبِهِۦ مَرَضٌ
وَقُلْنَ قَوْلًا مَّعْرُوفًا ﴿32﴾ وَقَرْنَ فِى بُيُوتِكُنَّ وَلَا تَبَرَّجْنَ
تَبَرُّجَ ٱلْجَٰهِلِيَّةِ ٱلْأُولَىٰ وَأَقِمْنَ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتِينَ ٱلزَّكَوٰةَ
وَأَطِعْنَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓ إِنَّمَا يُرِيدُ ٱللَّهُ لِيُذْهِبَ عَنكُمُ
ٱلرِّجْسَ أَهْلَ ٱلْبَيْتِ وَيُطَهِّرَكُمْ تَطْهِيرًا ﴿33﴾ وَٱذْكُرْنَ مَا يُتْلَىٰ
فِى بُيُوتِكُنَّ مِنْ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ وَٱلْحِكْمَةِ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ لَطِيفًا خَبِيرًا ﴿34﴾

(WANI ABU DAGA LADABAN DAKIN MA'AIKIN ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

28. Ya wannan Annabi Sallallahu alaihi wasallama, ka fada ga matayenka su tara sun nemi wani abu daga kayan ƙawar duniya abinda bashi dashi kace dasu inkun kasance kuna nufin rayuwar duniya da kayan adonta to kuzo in jiyar daku daɗi, jiyar daku daɗi na shika in sakeku shika kyakkyawa bada cutarwa gareku ba,

29. Inkun kasance kuna nufin Allah da Ma'aikinsa da gidan Lahira aljanna, haƙiƙa Ubangiji ya tanadi lada mai girma ga masu kyautatawar aiki daga cikinku, to sai suka zaɓi Lahira a kan duniya.

30. Yaku matayen Annabi Sallallahu alaihi wasallama, wacce tazo daga cikinkuda ɓama mabayyaniya za a ninninka mata azabaninki biyu, wannan ya kasance mai sauƙine bisa Ubangiji.

(WANI ABU DAGA LADABAN AHLUL-BAITI WATO IYALIN MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA, AKWAI AMBATON KULLE A CIKI)

31. Wacce tayi ɗa'a ga Allah da ma'aikinsa daga cikinku tayi aiki nagari mabata sakamakonta abin ninkawa biyu, Mun tanadi arziki maigirma a cikin Aljanna kari a kan wannan.

32. Ya matayen Annabi Sallallahu alaihi wasallama, baku kasance kamarɗaya daga mataye ba, in kunji tsoron Allah, kadaku ,rausaya magana ga mazaje bare wanda nufaƙa take cikin zuciyarsa yayi tsammani a cikinku, ku faɗi magana abar sani bada tausasawa ba.

(WAJABCIN KULLE GA MATAYEN MUSULMI)

33. Ku tabbata a cikin ɗakunanku kadaku ,bayyana irin bayyanar jahiliyya ta farko, wato abinda yake gaban Musulunci na daga kada kuyi gwaɗare da bayyana adonsu ga mazaje, bayyanawa kuma bayan Musulunci abin ambato ne a cikin aya daTace kadasu bayyana adonsu sai abinda ya bayyana daga gareta ku tsaya da salla daidai wadaida, kubada zakka, kubi Allah kubi manzonsa, Ubangiji yana nufin kawar da dauɗa daga garekune kawai yaku 'yan ɗakin Ma'aiki Sallallahu alaihi wasallama kuma ya tsarkake ku tsarkakewa.

34. Ku ambaci abinda ake karantawa daga ayoyin Allah (alƙur'an da hikima shine Alƙur'ani da Hadisi) a cikin ɗakunanku, haƙiƙa Ubangiji ya tabbata mai tausasawa ga waliyyansa, masani da dukkan halittarsa.

حزب

* إِنَّ الْمُسْلِمِينَ وَالْمُسْلِمَاتِ وَالْمُؤْمِنِينَ وَالْمُؤْمِنَاتِ وَالْقَانِتِينَ وَالْقَانِتَاتِ
وَالصَّادِقِينَ وَالصَّادِقَاتِ وَالصَّابِرِينَ وَالصَّابِرَاتِ وَالْخَاشِعِينَ وَالْخَاشِعَاتِ
وَالْمُتَصَدِّقِينَ وَالْمُتَصَدِّقَاتِ وَالصَّائِمِينَ وَالصَّائِمَاتِ وَالْحَافِظِينَ فُرُوجَهُمْ
وَالْحَافِظَاتِ وَالذَّاكِرِينَ اللَّهَ كَثِيرًا وَالذَّاكِرَاتِ أَعَدَّ اللَّهُ لَهُم مَّغْفِرَةً وَأَجْرًا عَظِيمًا (35)
وَمَا كَانَ لِمُؤْمِنٍ وَلَا مُؤْمِنَةٍ إِذَا قَضَى اللَّهُ وَرَسُولُهُ أَمْرًا
أَن تَكُونَ لَهُمُ الْخِيَرَةُ مِنْ أَمْرِهِمْ وَمَن يَعْصِ اللَّهَ وَرَسُولَهُ
فَقَدْ ضَلَّ ضَلَالًا مُّبِينًا (36) وَإِذْ تَقُولُ لِلَّذِي أَنْعَمَ اللَّهُ عَلَيْهِ
وَأَنْعَمْتَ عَلَيْهِ أَمْسِكْ عَلَيْكَ زَوْجَكَ وَاتَّقِ اللَّهَ وَتُخْفِي فِي نَفْسِكَ مَا اللَّهُ مُبْدِيهِ
وَتَخْشَى النَّاسَ وَاللَّهُ أَحَقُّ أَن تَخْشَاهُ فَلَمَّا قَضَى زَيْدٌ مِّنْهَا وَطَرًا
زَوَّجْنَاكَهَا لِكَيْ لَا يَكُونَ عَلَى الْمُؤْمِنِينَ حَرَجٌ فِي أَزْوَاجِ أَدْعِيَائِهِمْ
إِذَا قَضَوْا مِنْهُنَّ وَطَرًا وَكَانَ أَمْرُ اللَّهِ مَفْعُولًا (37) مَّا كَانَ عَلَى النَّبِيءِ
مِنْ حَرَجٍ فِيمَا فَرَضَ اللَّهُ لَهُ سُنَّةَ اللَّهِ فِي الَّذِينَ خَلَوْا مِن قَبْلُ
وَكَانَ أَمْرُ اللَّهِ قَدَرًا مَّقْدُورًا (38) الَّذِينَ يُبَلِّغُونَ رِسَالَاتِ اللَّهِ وَيَخْشَوْنَهُ
وَلَا يَخْشَوْنَ أَحَدًا إِلَّا اللَّهَ وَكَفَى بِاللَّهِ حَسِيبًا (39) * مَّا كَانَ مُحَمَّدٌ أَبَا أَحَدٍ
مِّن رِّجَالِكُمْ وَلَكِن رَّسُولَ اللَّهِ وَخَاتَمَ النَّبِيئِينَ وَكَانَ اللَّهُ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمًا (40)

ثمن

35. Haƙiƙa Musulmai maza da mata, da muminai maza da mata, da masu biyayya maza da mata, da masu gaskiya acikin imani maza da mata, da masu haƙuri a kan ɗa'a maza da mata, da masu tawali'u ga Allah maza da mata, da masu sadaka maza da mata, da masu azumi maza da mata, da masu kiyaye farjojinsu ga buran haram maza da mata, masu ambaton Allah da yawa maza da mata, Allah ya tanadi gafarar zunubai garesu, da lada maigirma bisa ɗa'o'i.

(ƘISSAR ZAINABU 'YAR JAHSHU TAREDA ZAIDU DAN HARISATA

36. Bazai halatta ga mumini ko mumina ba idan Allah (Ta'ala) da ma'aikinsa sun hukunta wani al'amari ya zama suna da zaɓi daga lamarinsu). Duk wanda ya saɓi Allah dama'aikinsa haƙiƙa ya ɓata, ɓata mabayyani [1].
37. Ambaci zamanin da kake faɗa ga wanda Allah yayi ni'ima gareshi (da Musulunci) kai kuma kayi ni'ima gareshi (da 'yanci Shine Zaidu ɗan Harisata ya kasance daga ribatattun jahiliyya, Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama ya sayeshiya 'yantashi, ya riƙe shi ɗa.) riƙe matarka gareka, kaji tsoron Allah (cikin shikanta) kana ɓoyewa a ranka abinda Allah mai bayyana Shine, (Shine cewa Allah yasanar dakai cewa da sannu zata zama ɗaya daga matayenka bayan Zaidu ya saketa,) kanajin tsoron mutane (suce ya auri matar ɗansa,) Ubangiji ne mafi cancanta kaji tsoronsa (a cikin kowane abu, kadaka damu da maganar mutane, sannan Zaidu ya saketa, ta gama idda, sai Ubangiji yace,) "Yayin da Zaidu ya biya buƙata daga gareta (ya zama bashi da wata buƙata a cikinta ya saketa, iddarta ta ƙare) sai Muka aura maka ita, (Manzon Allah ya tareda ita, ya ƙosar da Musulmi gurasa da nama ya aikata walima wacce bai taɓa irinta ba a cikin sauran matayensa) don kada a sami ƙuntatawa a cikin matayen 'ya'yansu na rana (idan suka biya buƙata daga garesu wato in sun gama dasu,) al'amarin Ubangiji ya kasance abin aikatawa.
38. Ba wani ƙunci ga Annabi a cikin abinda Allah ya halatta masa, al'adar Ubangiji ce acikin waɗanda suka wuce gabansa na daga Annabawa (Shine ba ƙunci garesu cikin wannan don yalwatawa garesu cikin aure, Annabi Dawuriu yana da mace ɗari (100), Annabi Sulaimanu yana da ɗari bakwai (700) da ƙwarƙwara ɗari (100) alaihi-mussalamu), al'amarin Ubangiji ya kasance ƙaddara, (wato hukunci abin hukuntawa).
39. Sune masu isarda aiken Ubangiji, masu tsoronsa, basa tsoron kowa sai Allah, (basa tsoron mutane cikin abinda Allah ya halatta musu. Ubangiji ya isa mai kiyayewa (ga ayyukan halittarsa mai lissafa musu ayyukansu).

(ƘARYATA YAN AHMADIYYA DA SHUGABANSU AHMADU GULAMU, YAYI DA'AWAR ANNABTAKA)

40. Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama, bai kasance uban ɗaya daga cikinku ba, ba uban Zaidu ne na yunɓu ba ubansa ne na addini, saboda haka auren Zainabu bazai haramta gareshi ba, shidai Manzon Allah ne cikamakin Annabawa ne, bazai kasance yanada wandazai zama Annabi bayansa ba, Ubangiji masanine da komai, yana daga gareshi cewa ba wani Annabi bayan Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama, 'idan Annabi Isa alaihissalamu ya sauka zaiyi hukunci da hukimcin Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama ne, Ahmadu Gulamu kuma ƙarya yake, haka duk wanda zaiyi da'awar Annabci ƙarya yake, har ranar alƙiyama.

1) Wannan aya ta sauka a Abdullahi dan JahsHu da 'yar uwarsa Zainabu, amma a cikin ƙissar an ambatacewa Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) yaganta a wani lokaci sai ƙaunarta ta afku cikin ransa, wannan ba mai dacewa bane a matsayin Annabi Sallallahu alaihi wasallama, saboda ganinta sai sha'awarta ta afku! wannan matsayin muminai ne da sauran jama'a, wannan bai dace da matsayin Annabci ba, ko mai cikakken imani ma bai dace dashi ba, (a duba sawii).

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا ٱذْكُرُوا ٱللَّهَ ذِكْراً كَثِيراً ﴿41﴾ وَسَبِّحُوهُ بُكْرَةً وَأَصِيلاً ﴿42﴾
هُوَ ٱلَّذِے يُصَلِّے عَلَيْكُمْ وَمَلَٰٓئِكَتُهُۥ لِيُخْرِجَكُم مِّنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ
وَكَانَ بِالْمُؤْمِنِينَ رَحِيماً ﴿43﴾ تَحِيَّتُهُمْ يَوْمَ يَلْقَوْنَهُۥ سَلَٰمٌ
وَأَعَدَّ لَهُمْ أَجْراً كَرِيماً ﴿44﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيٓءُ إِنَّآ أَرْسَلْنَٰكَ شَٰهِداً وَمُبَشِّراً
وَنَذِيراً ﴿45﴾ وَدَاعِياً إِلَى ٱللَّهِ بِإِذْنِهِۦ وَسِرَاجاً مُّنِيراً ﴿46﴾
وَبَشِّرِ ٱلْمُؤْمِنِينَ بِأَنَّ لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ فَضْلاً كَبِيراً ﴿47﴾
وَلَا تُطِعِ ٱلْكَٰفِرِينَ وَٱلْمُنَٰفِقِينَ وَدَعْ أَذَىٰهُمْ وَتَوَكَّلْ عَلَى ٱللَّهِ
وَكَفَىٰ بِاللَّهِ وَكِيلاً ﴿48﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا إِذَا نَكَحْتُمُ ٱلْمُؤْمِنَٰتِ
ثُمَّ طَلَّقْتُمُوهُنَّ مِن قَبْلِ أَن تَمَسُّوهُنَّ فَمَا لَكُمْ عَلَيْهِنَّ مِنْ عِدَّةٍ تَعْتَدُّونَهَا
فَمَتِّعُوهُنَّ وَسَرِّحُوهُنَّ سَرَاحاً جَمِيلاً ﴿49﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيٓءُ إِنَّآ أَحْلَلْنَا لَكَ
أَزْوَٰجَكَ ٱلَّٰتِے ءَاتَيْتَ أُجُورَهُنَّ وَمَا مَلَكَتْ يَمِينُكَ مِمَّآ أَفَآءَ ٱللَّهُ عَلَيْكَ
وَبَنَٰتِ عَمِّكَ وَبَنَٰتِ عَمَّٰتِكَ وَبَنَٰتِ خَالِكَ وَبَنَٰتِ خَٰلَٰتِكَ ٱلَّٰتِے هَاجَرْنَ
مَعَكَ وَٱمْرَأَةً مُّؤْمِنَةً إِن وَهَبَتْ نَفْسَهَا لِلنَّبِيِّ إِنْ أَرَادَ ٱلنَّبِيٓءُ أَنْ يَّسْتَنكِحَهَا
خَالِصَةً لَّكَ مِن دُونِ ٱلْمُؤْمِنِينَ قَدْ عَلِمْنَا مَا فَرَضْنَا عَلَيْهِمْ فِے أَزْوَٰجِهِمْ
وَمَا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُهُمْ لِكَيْلَا يَكُونَ عَلَيْكَ حَرَجٌ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُوراً رَّحِيماً ﴿50﴾

(KWADAITARWA BISA YAWAITA AMBATON ALLAH)

41. Yaku wađanda suka bada gaskiya, ku ambaci Allah ambato mai yawa, (duk abinda ake ambatonsa Zikirul- Lahi yana shiga cikin wannan umarni salla ce ko azumi ko zikirin Allah Ta'ala kamar bandiri ko waninsa yadda malamai suka tabbatar da wannan a cikin littattafansu hatta zikiran maulawiyya na mabiyan Shaihu Jalalurrumi, saboda Musulmi sun yi ijma'i a kan yarda da wađannan al'amura ga Arba-bul- Ahwali kamar yandasuyudi ya fađa
42. Ku tsarkake Allah Ubangiji safiya dayammaci.
43. Shine wandyake jinƙai garekuda Mala'ikunsa suna neman gafara gareku domin yafitar daku daga duffan kafirci izuwa hasken imani. Ubangiji ya tabbata mai jinƙai (ga muminai).

(LARABCI SHINE LUGAR CIKIN ALJANNA GA 'YAN ALJANNA)

44. Gaisuwa daga Allah Ta'ala ranar dasuke gamuwa dashi SALAMUN (da harshen Mala'iku, an ruwaito ga Ibn Abbasin cewa Larabci Shine lugar" yan aljanna a cikin aljanna), ya tanadi lada maigirma a garesu.

(KIRARI GA ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA DASUNA BAKWAI, DA IJAZA GA MURIDAI WACCE SHEHUNNAI SUKE MUSU, DA ALBISHIR GA MUMINAI CEWA SUNA DA FALALA MAIGIRMA)

45. Yakai wannan Annabi haƙiƙa Mu Mun aikoka mai shaida (ga wanda aka aikoka izuwa garesu) mai albishir (ga wanda yagasgata kada Aljanna) gargađi (ga wanda ya ƙaryatada wuta).
46. Mai kira izuwa bin Allah da izinin Allah, fitila mai haske (kamar fitila a cikin shiriya da ita)(1)
47. Yiwa muminai albishir cewa suna da falala maigirma daga Allah.
48. Kada kabi kafirai da munafukai (cikin abinda ya sađi shari'arka) ka rabu da cutarsu (kadaka saka musu a kanta, sai an umarceka cikinsu da umarni) ka dogara bisa Ubangiji (Shine ma'ishinka,) Allah ya isa abin dogara a gareshi.

(DĂDADAWA MATA KODA AN SAKESU)

49. Yaku wađanda suka bada gaskiya in kuka auri mataye muminai sannan kuka sakesu tun gaban baku sadu dasu ba, to ba wani abu na idda da kuke dashi a kansu da zaku kiyayetada tsarkakewa da waninta, to saiku jiyar dasu dađi (wato ku basu abinda zasuji dađi dashi in ba'a ambaci sadaki garesu ba, in kuwa an ambaci sadaki garesu to rabin abinda aka ambata ne ke garesu kawai ibn Abbas ne ya fađi haka, kuma Maliki da Shafi'i a kansu suke), ku sakesu saki kyakkyawa (bada cutarwa ba).

(WANI ABU DAGA KEBANTACCIYAR DARAJAR ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

50. Ya wannan Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) haƙiƙa Mu mun halatta matayenka agareka wađandaka basu sadakansu da abinda hannunka ya mallaka na daga abinda Allah ya taro shi gareka na daga kafirai ta ribacewa kamar (Safiyatu da Juwairatu) da'ya'yan baffanka da 'ya'ya mata na ammominka da 'ya'yaye mata na kawunka da 'ya'yayen mata na yakumobinka wađanda sukayi hijira tareda kai, (banda wađanda basuyi hijira ba) da mace mumina in ta bada kanta ga Annabi (Sallalla-hu alaihi wasallama) in Annabi yanufi ya aureta, bada sadaki ba, ta tsarkaka gareka bada sauran muminai ba, ka auretada lafazin kyauta bada sadaki ba). Mun san abinda Muka wajabta a garesu (muminai) a cikin matayensu na hukunce-hukunce, kadasu ƙara a kan mace huđu, kadasuyi aure saida waliyyi da shaidu da sadaki, hakana abinda hannunsu ya mallaka na kuyangi da saye da waninsa Shine kuyanga ta kasance halattacciyaga mana Ilakinta kamar Bakitabiya banda Bamagujiya banda Asniya, kuma a nemi kuɓutar mahaifanta gabanta don wato suduwa da ita kada a samu ƙunci a gareka a cikin auren. Ubangiji ya tabbata mai gafara ga abinda tsaruwa ga buransa ya wuyata, mai jinƙai ne dayalwata cikin wancananka.

1) Wanda shehunsa yayi masa ijaza da wani abu na ilimi haƙiƙa hanya ta sawwaƙa gareshi, wanda bashi da ijaza ya harđe da kansa ya wofintar da kansa da waninsa, duk hanyoyinsa zasu toshe - SAWI -

ربع

۞ تُرْجِي مَن تَشَآءُ مِنْهُنَّ وَتُـْٔوِيٓ إِلَيْكَ مَن تَشَآءُ وَمَنِ ٱبْتَغَيْتَ مِمَّنْ
عَزَلْتَ فَلَا جُنَاحَ عَلَيْكَ ذَٰلِكَ أَدْنَىٰٓ أَن تَقَرَّ أَعْيُنُهُنَّ وَلَا يَحْزَنَّ
وَيَرْضَيْنَ بِمَآ ءَاتَيْتَهُنَّ كُلُّهُنَّ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ مَا فِي قُلُوبِكُمْ
وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَلِيمًا ﴿51﴾ لَّا يَحِلُّ لَكَ ٱلنِّسَآءُ مِنۢ بَعْدُ
وَلَآ أَن تَبَدَّلَ بِهِنَّ مِنْ أَزْوَٰجٍ وَلَوْ أَعْجَبَكَ حُسْنُهُنَّ إِلَّا مَا مَلَكَتْ
يَمِينُكَ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ رَّقِيبًا ﴿52﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
لَا تَدْخُلُواْ بُيُوتَ ٱلنَّبِيِّ إِلَّآ أَن يُؤْذَنَ لَكُمْ إِلَىٰ طَعَامٍ غَيْرَ
نَٰظِرِينَ إِنَىٰهُ وَلَٰكِنْ إِذَا دُعِيتُمْ فَٱدْخُلُواْ فَإِذَا طَعِمْتُمْ
فَٱنتَشِرُواْ وَلَا مُسْتَـْٔنِسِينَ لِحَدِيثٍ إِنَّ ذَٰلِكُمْ كَانَ يُؤْذِي
ٱلنَّبِيَّ فَيَسْتَحْيِۦ مِنكُمْ وَٱللَّهُ لَا يَسْتَحْيِۦ مِنَ ٱلْحَقِّ
وَإِذَا سَأَلْتُمُوهُنَّ مَتَٰعًا فَسْـَٔلُوهُنَّ مِن وَرَآءِ حِجَابٍ
ذَٰلِكُمْ أَطْهَرُ لِقُلُوبِكُمْ وَقُلُوبِهِنَّ وَمَا كَانَ لَكُمْ أَن تُؤْذُواْ
رَسُولَ ٱللَّهِ وَلَآ أَن تَنكِحُوٓاْ أَزْوَٰجَهُۥ مِنۢ بَعْدِهِۦٓ أَبَدًا
إِنَّ ذَٰلِكُمْ كَانَ عِندَ ٱللَّهِ عَظِيمًا ﴿53﴾ إِن
تُبْدُواْ شَيْـًٔا أَوْ تُخْفُوهُ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمًا ﴿54﴾

51. Kana jinkirtar da wacce kaga dama daga matayenka, (ga buran ranarta,) kana taro wacce kaga dama daga cikinsu (kaje mata, wacce ka nema daga wađandaka janyesu daga rabon kwana, to babu laifi gareka a cikin nemanta, tara ta izuwa gareka shi yafi. Bayan rabon kwana ya kasance wajibi a gareshi, wannan bada zaɓinnan Shine yafi kusanci izuwa idondunansu tayi sanyi kuma ya zama baza suyi baƙin ciki basu yarda da abinda ka basu dukkansu. Allah yasan abinda yake zukatanku na daga al'amarin matada karkata izuwa sashinsu. Dahir, Mun baka zaɓi ne cikinsu don sauwaƙewa a gareka a cikin abinda kake nufi. Ubangiji ya tabbata masani da halittarsa mai jinkiri da azabarsa ga wanda ya kamaceta.

52. Mata basu halarta garekaba bayan wađannan da suka zaɓeka wala ka musanya wađansu mataye wasunsu, koda kyansu ya ƙayatar dakai sai abinda damshinka wato hannunka ya mallaka na kuyangi to wađannan zasu halatta gareka. Ya mallaki Mariya yaddar Allah ta tabbata gareta bayansu, ta haifa masa Ibrahimu Mu'azzamu, ya mutu a cikin rayuwar mahaifinsa Sallallahu alaihi wasallama. Ubangiji ya tabbata mai la'akari kan komai.

WAJABCIN TSARI A BISA MUMINAI WATO KULLE)

53. Yaku wađanda suka bada gaskiya, kadaku shiga đakunan Annabi Sallallahu alaihi wasallama sai anyi muku izini (a cikin shiga, Shine ace ku shigo) izuwa abinci (to, saiku shiga) bakuna masu sauraron nunarsa ba saidai in an kiraku ku shiga. Idan kukaci abinci wato ku watse kadaku zauna kuna masu sauraron hira (daga ba'alinku izuwa ba'ali,) wancananku zama ya kasance yana cutar Annabi (Sallallahu alaihi wasallama), to yana jinkunyarku (wato yafitar daku). Ubangiji baya barin gaskiya (sai yayi bayaninta). In zaku tambayi matan Annabi Sallallahu alaihi wasallama wani abin amfani, to ku tambaye su daga bayan shamaki, wancananku shi yafi tsarki ga zuciyarkuda zuciyarsu daga aukarwa a cikin tuhuma. Bai kasance halal a gareku ku cuci ma'aikin Allah da wani abu ba, wala ku auri matayensa bayansa har abada, wancananku ya kasance zunubi maigirma nan ga Allah.

54. Inkun bayyana wani abu ko kuka ɓoyeshi a cikin aurensu bayansa to, haƙiƙa Allah ya tabbata masanine da kowane abu, zaiyi muku sakamako a kansa.

ثمن

۞ لَّا جُنَاحَ عَلَيْهِنَّ فِىٓ ءَابَآئِهِنَّ وَلَآ أَبْنَآئِهِنَّ وَلَآ إِخْوَٰنِهِنَّ
وَلَآ أَبْنَآءِ إِخْوَٰنِهِنَّ وَلَآ أَبْنَآءِ أَخَوَٰتِهِنَّ وَلَا نِسَآئِهِنَّ
وَلَا مَا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُهُنَّ ۗ وَٱتَّقِينَ ٱللَّهَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ
عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ شَهِيدًا ﴿55﴾ إِنَّ ٱللَّهَ وَمَلَٰٓئِكَتَهُۥ يُصَلُّونَ
عَلَى ٱلنَّبِىِّ ۚ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ صَلُّوا۟ عَلَيْهِ وَسَلِّمُوا۟ تَسْلِيمًا ﴿56﴾
إِنَّ ٱلَّذِينَ يُؤْذُونَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ لَعَنَهُمُ ٱللَّهُ
فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ وَأَعَدَّ لَهُمْ عَذَابًا مُّهِينًا ﴿57﴾ وَٱلَّذِينَ يُؤْذُونَ
ٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ بِغَيْرِ مَا ٱكْتَسَبُوا۟ فَقَدِ ٱحْتَمَلُوا۟ بُهْتَٰنًا
وَإِثْمًا مُّبِينًا ﴿58﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِىُّ قُل لِّأَزْوَٰجِكَ وَبَنَاتِكَ وَنِسَآءِ
ٱلْمُؤْمِنِينَ يُدْنِينَ عَلَيْهِنَّ مِن جَلَٰبِيبِهِنَّ ۚ ذَٰلِكَ أَدْنَىٰٓ
أَن يُعْرَفْنَ فَلَا يُؤْذَيْنَ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿59﴾
۞ لَّئِن لَّمْ يَنتَهِ ٱلْمُنَٰفِقُونَ وَٱلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ وَٱلْمُرْجِفُونَ
فِى ٱلْمَدِينَةِ لَنُغْرِيَنَّكَ بِهِمْ ثُمَّ لَا يُجَاوِرُونَكَ فِيهَآ إِلَّا قَلِيلًا ﴿60﴾ مَّلْعُونِينَ ۖ
أَيْنَمَا ثُقِفُوٓا۟ أُخِذُوا۟ وَقُتِّلُوا۟ تَقْتِيلًا ﴿61﴾ سُنَّةَ ٱللَّهِ
فِى ٱلَّذِينَ خَلَوْا۟ مِن قَبْلُ ۖ وَلَن تَجِدَ لِسُنَّةِ ٱللَّهِ تَبْدِيلًا ﴿62﴾

ربع

55. Babu laifi a garesu a cikin iyayensu su shiga garesu da 'ya'yayensu, da 'yan uwansu, da 'ya'yayen "yan uwansu maza, da 'ya'yayen "yan uwansu mata wala mataye muminai su shiga garesu, wala abinda hannunsu ta mallaka na kuyangi da bayi, sa gansu suyi zance dasu bada shamaki ba. Kuji tsoron Allah yaku matayen Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) cikin abinda aka umarce ku dashi, Haƙiƙa Ubangiji ya tabbata mahalarci ga komai ba abinda yake ɓuya a gareshi.

(DAYAN RUKUNAN DARIKAR SUFAYE GUDA UKU, SALATI GA ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WA-SALLAMA, HAILALA DA ISTIGFARI)

56. Haƙiƙa Ubangiji dashi da Mala'kunsa suna yin salati ga Annabi (Sallallahu alaihi wasallama). Ya waɗanda suka bada gaskiYakuyi Salati a gareshi, kuyi gaisuwa gareshi gaisuwa (wato kuce; (ALLAH-HUMMA SALLI ALA SAYYIDINA MUHAMMADIN WASALLIM[1].

(HARAMCIN CUTAR ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA DA MUMINAI)

'Duk wanda ya cuci Annabi Sallallahu alaihi wasallama ya kafirta'.

57. Haƙiƙa waɗannan dasuke cutar Allah da ma'aikinsa (sune kafirai, suna siffanta Allah da abinda yake mai tsarki ne ga barinsa na daga ɗaukar shariki, da ƙaryata manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama).Allah ya tsine musu Albarka a duniya da lahira, ya tanadi azaba mai wulaƙantarwa a garesu Itace jahannama[2] ba. Amma sigar Salati ga Annabi tanada yawa, wanda yayi riƙo da kowace siga alheri maigirma zai sadu gareshi a mafificinta abinda aka sanya Alu da Sahabu a ciki. - sawi.

58. Waɗannan dasuke cutar muminai maza da mata bada abinda suka tsuwurwurta basuke jifansu da abinda basujiba basu ganiba, haƙiƙa sun lafta ƙarya da zunubi mabayyani ga kansu.

(SUTURTA AL'AURAR MATAYE)

59. Ya Annabi (Sallallahu alaika wasallama) ka faɗa ga mataycnka da 'ya'yaycnka matada matayen muminai su kusanta a kansu daga mayafansu (Shine bargo wanda mataye suke lullubadashi susaki sashensa a kan fuskokinsu idan zasu fito saboda buƙata tasu sai idaniya guda ɗaya), wancananka Shine mafi kusanci a kan a sansu wato a san cewa 'ya'yane baza a cucesu da damu ba, saɓanin kuyangi su kadasu rufe fuskokinsu. Munafukai sun kasance suna tattaresu, Ubangiji ya tabbata mai gafara (ga abinda ya wuce na daga barin suttura,) mai jinƙai (dasu in sun suturce jukkunansu).

(SAKAMAKON MUNAFIKAI DA TSAWA GA BARIN MUMMUNAN ZATO GA MUMINAI MAZA DA MATA)

60. wallahi idan munafikai basu hanu ga barin munafincinsu bada waɗannan da cuta (ta raunin imani) take cikin zukatansu, da musu baza jita-jita a Madina wato faɗinsu "Magauta sun zo muku, rundunar yaƙinku kuma an rusbasu (to in basu hanu ba) lalle zamu salladaka a kansu, sannan baza suyi maƙobtaka dakai ba a cikinta sai kaɗan sannan a fitar dasu.

61. Suna abin tsinewa albarka. Ko'ina aka dace dasu a ɗanke su a karkashe su karkashewa (wannan Shine hukuncin da akayi umarni a cikirsu).

1). Malamai sunyi Ittifaki a bisa wajabcin Salati ga Annabi Sallallahu alaihi wasalla-ma, sun saɓa a cikin ayyana wajab'cin. Maliku yace; tana wajabasau daya a rayuwar mutum, Shafi'i yace; tana wajaba J Tahiyar ƙarshe ta kowace salla, waɗansunsu kuma sukace; tana wajaba a dukkan mazauni sau ɗaya, waɗansu sukace; tana wajaba yayin ambatonsa, waɗansu sukace; yawaitawa daga gareshi yana wajaba ba tareda adadi ba. Duk-dukadai Salati ga Annabi al'amarinta maigirma ne, har ba'alin masana sukace:Tana sadarwa ga Allah ba tareda Shehi =

2) Ba shakka 'yan bidi'a na wannan zamani namu, wannan aya ta hau kansu tayi daidai wadaida. Suna cutar Allah da dangana jiha gareshi suna cewa, a sama yake ya harɗe kamar yadda mutum yake harɗewa. Suna cutar ma'aikin Allah da haramta ziyararsa da kafirta wanda yayi kamun ƙafa dashi koda wani Waliyyi daga cikin Auliya'ulLahi. Allah ya kiyashemu - Sanajiy

يَسْـَٔلُكَ اَلنَّاسُ عَنِ اِ۬لسَّاعَةِۖ قُلْ إِنَّمَا عِلْمُهَا عِندَ اَللَّهِۖ
وَمَا يُدْرِيكَۖ لَعَلَّ اَلسَّاعَةَ تَكُونُ قَرِيباًۖ ﴿63﴾ إِنَّ اَللَّهَ
لَعَنَ اَلْكَٰفِرِينَ وَأَعَدَّ لَهُمْ سَعِيراً ﴿64﴾ خَٰلِدِينَ فِيهَا أَبَداً
لَّا يَجِدُونَ وَلِيّاً وَلَا نَصِيراًۖ ﴿65﴾ يَوْمَ تُقَلَّبُ وُجُوهُهُمْ فِي اِ۬لنَّارِ يَقُولُونَ
يَٰلَيْتَنَا أَطَعْنَا اَللَّهَ وَأَطَعْنَا اَلرَّسُولَاۖ ﴿66﴾ وَقَالُواْ رَبَّنَا إِنَّا أَطَعْنَا سَادَتَنَا
وَكُبَرَآءَنَا فَأَضَلُّونَا اَلسَّبِيلَاۖ ﴿67﴾ رَبَّنَا ءَاتِهِمْ ضِعْفَيْنِ مِنَ
اَلْعَذَابِ وَالْعَنْهُمْ لَعْناً كَثِيراًۖ ﴿68﴾ يَٰٓأَيُّهَا اَلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَكُونُواْ
كَالَّذِينَ ءَاذَوْاْ مُوسَىٰ فَبَرَّأَهُ اُ۬للَّهُ مِمَّا قَالُواْۖ وَكَانَ عِندَ اَللَّهِ
وَجِيهاًۖ ﴿69﴾ يَٰٓأَيُّهَا اَلَّذِينَ ءَامَنُواْ اُ۪تَّقُواْ اُ۬للَّهَ وَقُولُواْ قَوْلاً سَدِيداً ﴿70﴾
يُصْلِحْ لَكُمْ أَعْمَٰلَكُمْ وَيَغْفِرْ لَكُمْ ذُنُوبَكُمْۖ وَمَن يُطِعِ
اِ۬للَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَقَدْ فَازَ فَوْزاً عَظِيماًۖ ﴿71﴾ * إِنَّا عَرَضْنَا اَلْأَمَانَةَ
عَلَى اَلسَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَالْجِبَالِ فَأَبَيْنَ أَن يَحْمِلْنَهَا وَأَشْفَقْنَ
مِنْهَاۖ وَحَمَلَهَا اَلْإِنسَانُ إِنَّهُۥ كَانَ ظَلُوماً جَهُولاً ﴿72﴾ لِّيُعَذِّبَ اَللَّهُ
اَلْمُنَٰفِقِينَ وَالْمُنَٰفِقَٰتِ وَالْمُشْرِكِينَ وَالْمُشْرِكَٰتِ وَيَتُوبَ اَللَّهُ
عَلَى اَلْمُؤْمِنِينَ وَالْمُؤْمِنَٰتِۖ وَكَانَ اَللَّهُ غَفُوراً رَّحِيماًۖ ﴿73﴾

ثمن

62. Al'adar Allah ce, Allah ya adanta wannan adantawa a cikin wađanda suka wuce gabanka a cikin munafukansu da muminai masu kwarmato, bazaka sami musanyawa ga al'adar Allah ba har abada. (Kada kayi baƙin ciki da samun munafukai cikin mutanenka, saboda wannan al'ada ce tsohuwa kamar yadda aka sami Musan Samiri cikin mutanen Annabi Musa da ƙarunu a mutanensa). (SAKAMAKON KAFIRAI)

63. Mutanen Makka suna tambayarka ga tashin Alƙiyama (yaushe zata kasance?) Cene "Saninta yana gurin Ubangiji". Wane abune yasanar dakai wato bakasan zamanin daza ayi tashin alƙiyama ba? Wata kila Sa'a zata kasance a kusa.

64. Haƙiƙa Ubangiji ya tsinewa kafirai ya nisanta su ya tanadi azabar wuta mai tsananin zafi garesu.

65. Masu dauwama a cikinta har abada bazasu samu mai kiyaye su daga gareta ba wala mai ijewa ga barinsu.

66. Ranar da ake juya fuskokinsu a cikin wuta su đora cewa, Ya dakace! Munbi Allah munbi Manzon Allah, suka fađa ga mabiyansu.

67. Sukace ya Ubangijinmu, mu mun bi shiwagabanmnmu da manya-manyanmu suka ɓatar damu hanyar gaskiya.

68. Ya Ubangijinmu basu ninki biyu na azabamu ka tsine musu albarka tsinewa mai yawa.

(GARGADE-GARGADE DA WA'AZE WA'AZE)

69. Ya wađanda suka bada gaskiya kadaku ,kasance tareda Annabinku kamar wadanda suka cuci Annabi Musa da fađinsu; Ba abindazai hana yayi wanka taredamu, saidon kasancewarsa mai kayan maza ne. Allah ya kuɓutar dashi daga abinda suka fađa (Shine ya ajiye tufarsa a kan dutse dan yayi wanka sai dutsen ya gudu yaje ya tsaya a tsakanin jama'a na Bani-Isra'ila sai Annabi Musa yaje ya riske shiya đauki tufarsa ya đaura, suka ganshi ba (udra) wato kumburi a cikin maraina wanda Hausawa suke cewa gwaiwa), ya kasance mai alfarma a gurin Allah .[1].

70. Yaku wađanda suka bada gaskiya, kuji tsoron Allah ku fađi magana ta gaskiya wacce take ta sosai.

71. Ya gyara muku ayyukanku, ya gafarta muku zunubanku. Wanda yabi Allah da Ma'aikinsa, haƙiƙa ya rabauta rabo maigirma izuwa matukar abin nemansa.

(AMANA TA TAKLIFI DA DAUKARTA, DA AMANA TA ASRARULLAHI TA'ALA WACCE TAKE KIRJIN ANNABAWA DA WALIYYAI)

72. Haƙiƙa Mu, Mun bijirar da amana (salloli da waninsu da ayyukan samun lada da aikin saɓo, Mun bijirar dasu) bisa sammai da ƙassaida duwarwatsu (an halitta musu fahinta ta furuci sukaƙi su đauke ta sukaji tsoron ta, mutum (wato Annabi Adamu) ya đauketa bayan an bijirar da ita gareshi. haƙiƙa Annabi Adamu ya kasance mai zalunta ga kansa da abinda ya đauka mai jahiltada ita.

73. Allah yayi hakane donya azabci munafukai maza da matada mushirikai maza da mata masu tozarta amana, ya karɓi tuba ga muminai maza da mata masu bada amana. Ubangiji ya tabbata mai gafara ga dukkan muminai, mai rahama garesu [2].

1) Kada a zaci cewa Annabi Musa yayi tsira-ra ne (uryanan) yadda al'aurarsa zata bayyana ga mutane. A'a. wato lalle yana saye da wani dan gajeren sutura wacce take bin jikinsa wacce zata hana a ga tsi-raicinsa. Amma tsiraici mummuna hara-mun ne a kowace shari'a, bazai yiwu mu-mini ma yayi tsiraici ba balle Annabin Allah. Yayiwu yana sanye da dan ƙaramin wando kamar gajeren wando wanda Manzon Allah yake dashi. Nayi Risala wacce na bayyana wannan magana a cikinta" yar karama; a neme ta a ga ci-kakken bayani. Yana daga cikin abinda aka cuci Ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wasalla-ma dashi cewa yayi rabo, sai wani mu-tum yace: shi wannan rabo ne wanda ba'a nufi Allah dashi ba", sai Annabi Sallalla-hu alaihi wasallama yayi fushi saboda wannan yace: "Allah yajikan Annabi Musa. Haƙiƙa an cuce shi da mafi yawa daga wannan, saiya daure." Bukhari ya ruwaito wannan Hadisin. - Sanajiy

2) Ance amana guda biyu ce: Amana ta tak-lifi da amana ta asirin Ubangiji. To ita wannan aya duk wađannan ma'anoni take nufi a ma'anar taklifi kowa yasanta. Amana ta asirin Allah, wannan ba kowa yasan ta basai Annabawa sai Waliyyai. Izuwa Manzon Allah Sallallahu alaihi wa-sallama yayi ishara da fađinsa: Abu Hu-rairata (R.A.) ya fađa : na karɓi birgami biyu daga Ma'aikin Allah (S.A.W.) na daga ilimi, ilimin da yake kamar Lu'ulu,i Abin boyewa cikin kwasfo : Amma na far-ko na daidaitashi ga mutane, Amma dayan dana bayyana wani abu na daga gareshi da kun yanke min wannan makogwaro nawa. (Bukhari ya ruwaito shi) Zainul Abidina yace : Ya jama'a, da yawa lu'ulu'in ilimi da zan bayyana shi da Ance ni ina daga cikin masu bautar guma-ka da mutane Musulmi sun halatta jinina, sun ganin abinda suke aikatawa kyakkya-wane.

34 سُورَةُ سَبَإٍ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ أَرْبَعٌ وَخَمْسُونَ ءَايَةً 54

بِسْمِ اِ۬للَّهِ اِ۬لرَّحْمَٰنِ اِ۬لرَّحِيمِ

اَ۬لْحَمْدُ لِلَّهِ اِ۬لذِے لَهُۥ مَا فِے اِ۬لسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِے اِ۬لْأَرْضِۖ وَلَهُ اُ۬لْحَمْدُ
فِے اِ۬لْأٓخِرَةِۖ وَهْوَ اَ۬لْحَكِيمُ اُ۬لْخَبِيرُۖ 1 يَعْلَمُ مَا يَلِجُ فِے اِ۬لْأَرْضِ
وَمَا يَخْرُجُ مِنْهَا وَمَا يَنزِلُ مِنَ اَ۬لسَّمَآءِ وَمَا يَعْرُجُ فِيهَاۖ وَهْوَ اَ۬لرَّحِيمُ
اُ۬لْغَفُورُۖ 2 وَقَالَ اَ۬لذِينَ كَفَرُواْ لَا تَأْتِينَا اَ۬لسَّاعَةُۖ
قُلْ بَلَيٰ وَرَبِّے لَتَأْتِيَنَّكُمْ عَٰلِمِ اِ۬لْغَيْبِ لَا يَعْزُبُ عَنْهُ مِثْقَالُ ذَرَّةٖ
فِے اِ۬لسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِے اِ۬لْأَرْضِۖ وَلَا أَصْغَرُ مِن ذَٰلِكَ وَلَا أَكْبَرُ
إِلَّا فِے كِتَٰبٖ مُّبِينٖ 3 لِّيَجْزِيَ اَ۬لذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ اُ۬لصَّٰلِحَٰتِۖ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُم
مَّغْفِرَةٞ وَرِزْقٞ كَرِيمٞۖ 4 وَالذِينَ سَعَوْ فِے ءَايَٰتِنَا مُعَٰجِزِينَ أُوْلَٰٓئِكَ
لَهُمْ عَذَابٞ مِّن رِّجْزٍ أَلِيمٞۖ 5 وَيَرَى اَ۬لذِينَ أُوتُواْ اُ۬لْعِلْمَ اَ۬لذِےٓ أُنزِلَ إِلَيْكَ
مِن رَّبِّكَ هُوَ اَ۬لْحَقُّ وَيَهْدِےٓ إِلَيٰ صِرَٰطِ اِ۬لْعَزِيزِ اِ۬لْحَمِيدِۖ 6
* وَقَالَ اَ۬لذِينَ كَفَرُواْ هَلْ نَدُلُّكُمْ عَلَيٰ رَجُلٖ يُنَبِّئُكُمْ إِذَا مُزِّقْتُمْ كُلَّ مُمَزَّقٍ إِنَّكُمْ لَفِے خَلْقٖ جَدِيدٍۖ 7 ربع

Suratu Saba'i

A Makka Aka. Saukar Da Ita Ayoyinta Hamsin Da Hudu (54)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagabadaya mai jinƙan muminai a Lahira a keɓe

(KIRARI GA ALLAH SUBHANAHU WATA'ALA TSARKI YA ISAR MASA DA TABBATAR DA TASHIN ALKIYA-MA DA SABUBBAN TASHIN, DA RADDI GA MASU MUSUNTA)

1. Dukkan yabo ya tabbata ga Allah, wanda abinda ke cikin sammai da ƙassai yake mallaka tasa. Yabo yana gareshi a Lahira kamar yadda yake gareshi a duniya, Waliyyansa zasu gode masa idan suka shiga aljanna. Shine gwani a cikin aikinsa kwararre da sanin halittarsa.
2. Yasan abinda yake shiga cikin ƙasa (kamar ruwa da waninsa) da abinda yake fitowa daga gareta (kamar tsiri da waninsa,) da abinda yake sakkowa daga sama (nadaga sabubban arziki da waninsa) da abinda yake hawa cikinta (na aiki nagari da waninsa). Shine mai rahama (ga Waliyyansa) mai gafara (garesu).
3. Waɗanda suka kafirtada ayoyinmu sukace "Ba alƙiyama", cenc (dasu) "Haba! Na rantse da Ubangiji lalle za tazo muku ne". Masanin asirin fake misalin kwayar komayyabata fakuwa ga barinsa a cikin sammai, wala a cikin ƙassai, wala mafi karan-ta daga wannan, wala mafi girma daga wancananka face yana cikin Littafi maigirma (Shine LAUHUL-MAHFUZU).
4. Domin ya saka wa waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru, waɗancananka suna da lada maigirma da gafara (a Aljanna).
5. Waɗanda sukayi ƙoƙari a cikin bata ayoyinmu (Alƙur'ani) suna masu tsere Mana (saboda zatonsu baza ayi tashin alƙiyama bakuma ba azaba). Waɗancananka azabadaga mummunar azaba mai raɗaɗi tana garesu.
6. Waɗandaka basu' ilimi kuwa (muminai Ahlul-Kitabi kamar Abdullahi Bin Salamin da abokansa) suna ganin abinda aka saukar gareka daga Ubangijinka. Alƙur'ani Shine gaskiya, kuma yana shiryarwa izuwa tafarki madaidaci abin godewa.
7. Waɗanda suka kafirta sukace (ba'alinsu yace da ba'ali a bisa jahar ban mana ki,) "Barna shiryar daku ,ba" a bisa mutum (suna nufin Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) dazai baku labari cewa, ku in an kerkece ku kerkecewa haƙiƙa ku kuna cikin halitta sabuwa.

أَفْتَرَىٰ عَلَى اَ۬للَّهِ كَذِباً اَمْ بِهِۦ جِنَّةٌۢ بَلِ اِ۬لذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ
بِالَاخِرَةِ فِي اِ۬لْعَذَابِ وَالضَّلَٰلِ اِ۬لْبَعِيدِۖ ﴿8﴾ أَفَلَمْ يَرَوْاْ إِلَىٰ
مَا بَيْنَ أَيْدِيهِمْ وَمَا خَلْفَهُم مِّنَ اَ۬لسَّمَآءِ وَالَارْضِۖ إِن نَّشَأْ
نَخْسِفْ بِهِمُ اُ۬لَارْضَ أَوْ نُسْقِطْ عَلَيْهِمْ كِسْفاً مِّنَ اَ۬لسَّمَآءِۖ
إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةً لِّكُلِّ عَبْدٍ مُّنِيبٍۖ ﴿9﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا دَاوُۥدَ
مِنَّا فَضْلاً يَٰجِبَالُ أَوِّبِي مَعَهُۥ وَالطَّيْرَۖ وَأَلَنَّا لَهُ اُ۬لْحَدِيدَ ﴿10﴾
أَنِ اِ۪عْمَلْ سَٰبِغَٰتٍ وَقَدِّرْ فِي اِ۬لسَّرْدِۖ وَاعْمَلُواْ صَٰلِحاًۖ
إِنِّي بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌۖ ﴿11﴾ وَلِسُلَيْمَٰنَ اَ۬لرِّيحَ غُدُوُّهَا شَهْرٌ
وَرَوَاحُهَا شَهْرٌۖ وَأَسَلْنَا لَهُۥ عَيْنَ اَ۬لْقِطْرِۖ وَمِنَ اَ۬لْجِنِّ مَنْ يَّعْمَلُ بَيْنَ
يَدَيْهِ بِإِذْنِ رَبِّهِۦۖ وَمَنْ يَّزِغْ مِنْهُمْ عَنْ أَمْرِنَا نُذِقْهُ مِنْ عَذَابِ
اِ۬لسَّعِيرِۖ ﴿12﴾ يَعْمَلُونَ لَهُۥ مَا يَشَآءُ مِن مَّحَٰرِيبَ وَتَمَٰثِيلَ وَجِفَانٍ
كَالْجَوَابِ وَقُدُورٍ رَّاسِيَٰتٍۖ اِ۪عْمَلُواْ ءَالَ دَاوُۥدَ شُكْراًۖ وَقَلِيلٌ مِّنْ
عِبَادِيَ اَ۬لشَّكُورُۖ ﴿13﴾ فَلَمَّا قَضَيْنَا عَلَيْهِ اِ۬لْمَوْتَ مَا دَلَّهُمْ عَلَىٰ
مَوْتِهِۦ إِلَّا دَآبَّةُ اُ۬لَارْضِ تَأْكُلُ مِنسَاتَهُۥۖ فَلَمَّا خَرَّ تَبَيَّنَتِ اِ۬لْجِنُّ
أَن لَّوْ كَانُواْ يَعْلَمُونَ اَ۬لْغَيْبَ مَا لَبِثُواْ فِي اِ۬لْعَذَابِ اِ۬لْمُهِينِ ﴿14﴾

8. "Shin ya ƙagi ƙarya ne bisa Allah (a cikin wancananka,) koko hauka ne dashi?" Sai Ubangiji yace: A'a, waɗanda basu bada gaskiya da Lahira (wacce ta kunshi tashin ƙiyama) suna cikin azabada bata mai nisa (ga barin gaskiya a duniya).
9. Shin basuyiduba bane izuwa abinda yake gabansu da bayansu da cikin ƙasa? In Mun ga dama sai Mu kisfe ƙassai dasu, Jko Mu mso yanki na sammai a kansu, haƙiƙa akwai aya a cikin wancananka abin gani ga dukkan bawa mai koma wa ga Ubangijinsa.

(FALALAR ANNABI DAWURIU, DA ZIKIRIN DUWARWATSU, DA HARSHEN MAGANA, DA TSUNTSAYE)

10. Haƙiƙa Mun baiwa Annabi Dawuriu falala daga garemu, annabtada Littafi. Mun ce "Yaku duwatsu ku rangada murya tare dashi Dawuriu da Tashibi, Yaku tsuntsaye ku ma ku rangada murya tare dashi kuna tasbihi", Muka tausasa masa bakin ƙarfe (ya kasance a hannunsa kamar gayan fura).
11. Muka ce, aikata sulaka macika saƙa da masu ɗaurata zasu ja ta a ƙasa (daga wannan bakin karfen,) kayi gwaninta a cikin shirya sulakan da zata dace da ƙawanyoyinta, ku aikata aiki nagari tare dashi. Ni ina ganin abinda kuke aikatawa (zan saka muku dashi)".
12. Mun hore iska ga Annabi Sulaimanu wato jijjifinta har izuwa karyewar rana, yammacinta izuwa karyewar rana wata guda. Mun narka masa idaniyar tagul-la (aka gudanar da ita kwana uku kamar gudun ruwa) a cikin mutane izuwa yau, yana daga abinda aka baiwa Annabi Su-laimanu,) akwai daga aljannu waɗanda suke aiki nan gaba gareshi, da umarnin Ubangijinsa, wanda duk ya karkace daga cikinsu ga barin umarninmu da mukayi da a bi shi, Ma ɗanɗana masa daga azabar wutar Lahira data duniya shine (Mala'ika ya doke shi da bulala, duka da zata kone shi).
13. Suna aikata masa aiki wanda yake so na gingine wanda ake hawa a garetada matattakala (tsani) da hotuna (na ta gulla da gilas da gogaggun dutse. Amfani da hotuna bai kasance hara-mun ba a shari'arsa) da damna, wato tafki na ruwa kamar daro wadda kamar mutum dubu (1,000) tana iyaci daga gareta, da tukwane matabbata suna da ƙafafuwa waɗanda basa motsi, ana samo ta daga duwarwatsu a Yaman ana hawa garetada tsanunnuka). Sai Muka ce, "Kuyi aiki yaku iyalan Dawuriu don godiyaga Ubangiji. kaɗan ne ƙwarai masu godiya daga cikin bayina".
14. Yayin da Muka hukunta mutuwa ga Annabi Sulaimanu (ya zama yana dogare a kan sandarsa shekara guda aljanu suna ta aikace-aikace masu wuya na al'adarta bata san ya mutu ba har saida gara ta cinye sandarsa ya faɗi yana matacce,) babu abinda ya shiryar dasu a bisa mutuwarsa, sai dabba (wato gara) mai cinyewa data cinye sandarsa yayin daya faɗi yana matacce. Aljanu suka tabbatacewa su dasun kasance suna sanin gaibu (wato abinda ya faku ga barinsu na mutuwar Annabi Sulaimanu,) da basu zama a cikin wahala mai waulakantarwa ba.

(ƘISSAR SABA'U DA BARKEWAR DANGARAMA)

ثمن

۞ لَقَدْ كَانَ لِسَبَإٍ فِي مَسَٰكِنِهِمْ ءَايَةٌ جَنَّتَانِ عَن يَمِينٍ وَشِمَالٍ
كُلُوا۟ مِن رِّزْقِ رَبِّكُمْ وَاشْكُرُوا۟ لَهُۥ بَلْدَةٌ طَيِّبَةٌ وَرَبٌّ غَفُورٌ ﴿15﴾
فَأَعْرَضُوا۟ فَأَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ سَيْلَ ٱلْعَرِمِ وَبَدَّلْنَٰهُم بِجَنَّتَيْهِمْ جَنَّتَيْنِ
ذَوَاتَيْ أُكْلٍ خَمْطٍ وَأَثْلٍ وَشَيْءٍ مِّن سِدْرٍ قَلِيلٍ ﴿16﴾
ذَٰلِكَ جَزَيْنَٰهُم بِمَا كَفَرُوا۟ وَهَلْ يُجَٰزَىٰٓ إِلَّا ٱلْكَفُورُ ﴿17﴾
وَجَعَلْنَا بَيْنَهُمْ وَبَيْنَ ٱلْقُرَى ٱلَّتِي بَٰرَكْنَا فِيهَا قُرًى ظَٰهِرَةً
وَقَدَّرْنَا فِيهَا ٱلسَّيْرَ سِيرُوا۟ فِيهَا لَيَالِيَ وَأَيَّامًا ءَامِنِينَ ﴿18﴾
فَقَالُوا۟ رَبَّنَا بَٰعِدْ بَيْنَ أَسْفَارِنَا وَظَلَمُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ فَجَعَلْنَٰهُمْ
أَحَادِيثَ وَمَزَّقْنَٰهُمْ كُلَّ مُمَزَّقٍ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ
لِّكُلِّ صَبَّارٍ شَكُورٍ ﴿19﴾ وَلَقَدْ صَدَقَ عَلَيْهِمْ إِبْلِيسُ ظَنَّهُۥ
فَاتَّبَعُوهُ إِلَّا فَرِيقًا مِّنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿20﴾ وَمَا كَانَ لَهُۥ عَلَيْهِم
مِّن سُلْطَٰنٍ إِلَّا لِنَعْلَمَ مَن يُؤْمِنُ بِالْأَخِرَةِ مِمَّنْ هُوَ مِنْهَا
فِي شَكٍّ وَرَبُّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ حَفِيظٌ ﴿21﴾ قُلُ ادْعُوا۟ ٱلَّذِينَ زَعَمْتُم
مِّن دُونِ ٱللَّهِ لَا يَمْلِكُونَ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِي ٱلْأَرْضِ
وَمَا لَهُمْ فِيهِمَا مِن شِرْكٍ وَمَا لَهُۥ مِنْهُم مِّن ظَهِيرٍ ﴿22﴾

15. Haƙiƙa aya ta tabbata ga Saba'u (kabila ce da aka ambace ta daga kakansu daga Larabawa a cikin guraren zamansu na Ya-man). Akwai aya mai shiryarwa a bisa ikon Allah. Gonaki ne guda biyu dama da hauni (na daga zazansu, (Ance dasu,) "Kuci daga arzikin Ubangijinku, ku gode masa saboda abinda yaci daku ,na daga ababan ni'ima), ita ƙasa ce daddaɗa (ba ƙasar gishid a cikinta, basauro, bakudin cizo, bakunama, ba macijiya, idan baƙo ya wuce a cikin tufarsa akwai kwarkwata sai kwarkwatar duk su mutu saboda daɗin iskarta). Allah Ubangiji ne mai yawan gafara.

16. Sai sukabijirce ga barin godiy-arsa, sukabitilce masa, Muka aiko kunzumin dangarama a kansu, (sai suka ga ya hallakar da gonarsu), Muka musanya musu maimakan gonarsu guda biyu, gona guda biyu, ma'abota abinci mai maƙaƙi, da gorubada wani abu ƙanƙani na magarya.

17. Wancananka (musanyawan nan) Mun sauya musune saboda kafircinsu. Ba kowa ne ake masa irin wannan sakamako basai kafiri

18. Mun sanya tsakanin Saba'u alhali suna Yaman da tsakanin alƙaryatun da Mukayi albarka a cikinta (da ruwa da bishiyoyi Itace alƙaryatun Sham wacce suke tafiya izuwa gareta saboda ciniki). Mun sanya alƙaryu sadaddu (tun daga Yaman izuwa Sham). Mun ƙaddara tafiya a cikinta (inda zasuyibaccin rana a guda ɗaya, su kwana a ɗayar har izuwa ƙarewar tafiyarsu, basa bukata a cikinta izuwa daukar guzuri ko ruwa, Mun ce dasu) "Ku tafi a cikintada rairai daranaiku kuna amintattu, (ba kwa tsoro a cikinta, wala a cikin rana).

19. Sukace Ubangiji nisanta tsakanin tafiyarmu (izuwa Sham, wato ka sa ta jazzai" donsuyitunkaho ga fuƙara'u da hawa busashe da ɗaukar guzuri da ruwa,) suka butulce wa ni'ima, suka zalunci kawukansu da kafirci, Muka mayar dasu labarai ga wanda yake bayansu, Muka rarrabasu a cikin gamruwa dukkan rarrabawa. haƙiƙa akwai iznace-iznace cikin wancananka abin ambato ga dukkan mai haƙuri (ga barin sabon Allah, mai godiya a kan ni'imomi.

20. Haƙiƙa Iblis yagasgata musu (kafirai) zatonsu (Shine cewa in ya halakar dasu zasu bi shi, to sai sukabi shi din. Sai zatonsu yagasgata,) saidai wadansu jama'a daga muminai basu bi shiba,

21. Kuma basu da hujja, wato bamu yi wannan basai don Mu nuna wanda ya bada gaskiya da Lahira daga wanda yake cikin kokwanto daga gareta, ma saka wa kowanne daga cikinsu. Ubangijinka mai la'akari ne a kan komai, mai kiyayewa ne.

(TUTSIYE MUSHIRIKAI DA TAKURA MUSU A CIKIN RUKON WANIN ALLAH IYAYEN-GIJI MASU CETO A GARESU)

22. (Ya Annabi Muhammadu,) gaya» wa (kafiran Makka) su kira waɗanda suke bautawa ba Allah ba (donsu amfane su da iyawarsu. Sai Ubangiji yace;) Basu mallaki misalin ƙwayar zan-a bana hairi. ko sharri a cikin samai ko ƙassai, kuma ta rayyabata kasance garesu ba a cikin sammai da ƙassai, ubangiji bashi da wani mataimaki a cikin iyayen giji.

وَلَا تَنفَعُ ٱلشَّفَٰعَةُ عِندَهُۥٓ إِلَّا لِمَنْ أَذِنَ لَهُۥ حَتَّىٰٓ إِذَا فُزِّعَ عَن
قُلُوبِهِمْ قَالُواْ مَاذَا قَالَ رَبُّكُمْ قَالُواْ ٱلْحَقَّ وَهُوَ ٱلْعَلِيُّ ٱلْكَبِيرُ ﴿23﴾
۞ قُلْ مَن يَرْزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ قُلِ ٱللَّهُ
وَإِنَّآ أَوْ إِيَّاكُمْ لَعَلَىٰ هُدًى أَوْ فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿24﴾
قُل لَّا تُسْـَٔلُونَ عَمَّآ أَجْرَمْنَا وَلَا نُسْـَٔلُ عَمَّا تَعْمَلُونَ ﴿25﴾
قُلْ يَجْمَعُ بَيْنَنَا رَبُّنَا ثُمَّ يَفْتَحُ بَيْنَنَا بِٱلْحَقِّ وَهُوَ ٱلْفَتَّاحُ
ٱلْعَلِيمُ ﴿26﴾ قُلْ أَرُونِىَ ٱلَّذِينَ أَلْحَقْتُم بِهِۦ شُرَكَآءَ كَلَّا بَلْ هُوَ
ٱللَّهُ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿27﴾ وَمَآ أَرْسَلْنَٰكَ إِلَّا كَآفَّةً
لِّلنَّاسِ بَشِيرًا وَنَذِيرًا وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿28﴾
وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلْوَعْدُ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿29﴾
قُل لَّكُم مِّيعَادُ يَوْمٍ لَّا تَسْتَـْٔخِرُونَ عَنْهُ سَاعَةً
وَلَا تَسْتَقْدِمُونَ ﴿30﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَن نُّؤْمِنَ بِهَٰذَا ٱلْقُرْءَانِ
وَلَا بِٱلَّذِى بَيْنَ يَدَيْهِ وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذِ ٱلظَّٰلِمُونَ مَوْقُوفُونَ عِندَ رَبِّهِمْ
يَرْجِعُ بَعْضُهُمْ إِلَىٰ بَعْضٍ ٱلْقَوْلَ يَقُولُ ٱلَّذِينَ ٱسْتُضْعِفُواْ
لِلَّذِينَ ٱسْتَكْبَرُواْ لَوْلَآ أَنتُمْ لَكُنَّا مُؤْمِنِينَ ﴿31﴾

حزب

23. Ceto bata amfani nan ga Allah Ubangiji (Ya faɗi wannan ne don faɗinsu cewa iyayen gijinsu tana ceto nan ga Allah) sai ga wanda Allah yayi masa izini da ceto, har yayin da aka kau da tsoro daga zukatansu da izini a cikin yin ceton, sai sashinsu yace da sashi (don albishir,) "Me Ubangijinku yace a cikin ceto?" Sai sukace "Ya faɗi gaskiya, Ubangiji Shine madaukaki maigirma."
24. Gaya musu, "Wanene mai azur-taku (ruwa) daga sammai ko (tsiri daga) ƙasa," Cene (dasu) "Allah ne, in basu faɗi haka ba, don ba wani jawabin sai shi, Haƙiƙa Mu ko ku, muna kan shiriyako cikin bata mabayyani.(Akwai tausasawa dasu a cikin ibhami wanda yake cikin wannan aya mai kiransu izuwa imani, in Allah yayi musu mu-wafuƙa izuwa haka).
25. Cene!'Baza a tambaye ku abinda muka aikata na zunubi bakuma baza a tambaye mu ga abinda kuke aikatawa ba, (saboda mu ba ruwanmu da ku)".
26. Cene Ubangijmmu zai hada tsakaninmu ranar alƙiyama, san-nan yayi hukunci tsakaninmu da gaskiya, (ya shigar da masu gaskiya aljanna, ya shigar da makaryata wuta). Shine mai hukunci, masani (da abindazaiyi hukunci dashi).
27. Cene dasu, "Ku nuna mini waɗanda kuka riskar dasu abokan tarayya dashi a cikin bauta (Kalla) Hir! (tsawa ne garesu daga kudure shariki ga Allah). Bari! Shine Allah mai rinjaye (a kan al'amarinsa) gwani (a cikin shirinsa na halitta, bashi da shariki a cikin mulkinsa).

(GAMAWAR AIKENSA SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA IZUWA DUK DUNIYA)

28. Bamu aikoka ba face kana mai gamawa da aike ga dukkan talikai, kana mai albishir (ga muminai da Aljanna) mai gargadi (ga kafirai da azaba). Saidai yawancin mutane (kafiran Makka) basu san haka ba.
29. Suna cewa, "Yaushe ne wannan alƙawari (na azaba) inkun ka-sance magasgata (a cikinsa?)"
30. Cene (dasu "Kuna da alƙawarin rana wanda bazakuyi jinkiri ga barinsa basa'a ɗaya wala gabata a kansa, (Shine ranar Alƙiyama).
31. Waɗanda suka kafirta (mutanen Makka) sukace "Bazamu bada gaskiya da wannan Alƙur'ani ba wala da wanda yake gaba gareshi, (kamar Attaura da Linjila masu shiryarwa bisa tashin Alƙiyama. Saboda sunyi musun sa sai Ubangiji yace dasu, "Ya Muhammadu Sallallahu alaika wasallama, Da kana dubazama-nin da kafirai akc tsayar dasu nan ga Ubangijinsu, ba'alinsu yana komar da magana izuwa ba'ali waɗanda suke raunana (sune mabiya) suna faɗa ga waɗanda sukayi girman kai (sune shiwagabanninsu. suna ce musu) Ba don kun hana mu ga barin imani bada mun kasance masu bada gaskiya (ga Annabi Sallallahy alaihi wasallama).

قَالَ اَ۬لذِينَ اَ۟سْتَكْبَرُواْ لِلذِينَ اَ۟سْتُضْعِفُوٓاْ أَنَحْنُ صَدَدْنَٰكُمْ
عَنِ اِ۬لْهُد۪يٰ بَعْدَ إِذْ جَآءَكُم بَلْ كُنتُم مُّجْرِمِينَ ﴿32﴾ وَقَالَ اَ۬لذِينَ
اَ۟سْتُضْعِفُواْ لِلذِينَ اَ۟سْتَكْبَرُواْ بَلْ مَكْرُ اُ۬ليْلِ وَالنَّهَارِ إِذْ تَأْمُرُونَنَآ
أَن نَّكْفُرَ بِاللَّهِ وَنَجْعَلَ لَهُۥٓ أَندَاداٗۖ وَأَسَرُّواْ اُ۬لنَّدَامَةَ لَمَّا
رَأَوُاْ اُ۬لْعَذَابَۖ وَجَعَلْنَا اَ۬لْأَغْلَٰلَ فِےٓ أَعْنَاقِ اِ۬لذِينَ كَفَرُواْۖ
هَلْ يُجْزَوْنَ إِلَّا مَا كَانُواْ يَعْمَلُونَۖ ﴿33﴾ * وَمَآ أَرْسَلْنَا فِے قَرْيَةٖ
مِّن نَّذِيرٍ اِلَّا قَالَ مُتْرَفُوهَآ إِنَّا بِمَآ أُرْسِلْتُم بِهِۦ كَٰفِرُونَۖ ﴿34﴾
وَقَالُواْ نَحْنُ أَكْثَرُ أَمْوَٰلاٗ وَأَوْلَٰداٗ وَمَا نَحْنُ بِمُعَذَّبِينَۖ ﴿35﴾
قُلْ إِنَّ رَبِّےَ يَبْسُطُ اُ۬لرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقْدِرُۖ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ
اَ۬لنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَۖ ﴿36﴾ وَمَآ أَمْوَٰلُكُمْ وَلَآ أَوْلَٰدُكُم بِالتِے
تُقَرِّبُكُمْ عِندَنَا زُلْف۪يٰٓ إِلَّا مَنْ ءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحاٗ فَأُوْلَٰٓئِكَ
لَهُمْ جَزَآءُ اُ۬لضِّعْفِ بِمَا عَمِلُواْ وَهُمْ فِے اِ۬لْغُرُفَٰتِ ءَامِنُونَۖ ﴿37﴾ وَالذِينَ
يَسْعَوْنَ فِےٓ ءَايَٰتِنَا مُعَٰجِزِينَ أُوْلَٰٓئِكَ فِے اِ۬لْعَذَابِ مُحْضَرُونَۖ ﴿38﴾
قُلْ إِنَّ رَبِّےَ يَبْسُطُ اُ۬لرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ وَيَقْدِرُ لَهُۥۖ
وَمَآ أَنفَقْتُم مِّن شَےْءٖ فَهْوَ يُخْلِفُهُۥۖ وَهْوَ خَيْرُ اُ۬لرَّٰزِقِينَۖ ﴿39﴾

ثمن

32. Wađanda sukayi girftian kai suka fađa ga wađanda aka ga ƙanƙantarsu "Shin Mune muka tarc ku ga barin shiriya bayan tazo muku?" A'a, bari! Kun kasance masu laifi ne a cikin kawukanku kawai.
33. Wađanda aka ga rauninsu suka fađa ga wađanda sukayi girman kai, bari makircin dare da rana f ne (đa kuke mana) yayin da kuke umarnin mu da mu kafirtada Allah, mu sanya masa ababan tarayya, wađannan jama'a guda biyu suka ɓoye nadama, (wato kowanne ya ɓoye nadamarsa ga buran dan'uwansa na dama bisa barin bada gaskiya) yayin da suka ga azaba Mun sanya kukumai cikin wuyayin wađanda suka kafirta a cikin wuta, ba a saka musu sai sakamakon abinda suka kasance suna aikatawa a duniya.
34. Bamu aiko wani mai gargađi ba a cikin alƙarya face shiwagabanninta, masu morewa jin dađi, (face) sunce, "Mu mun kafirce da abinda aka aikokuda ahi".
35. Kuma su ce, "Mune muka fi ya-wan dukiya da 'ya'ya (daga wađanda suka bada gaskiya), to mu bamu kassance ababan yiwa azaba ba".
36. Cene, " haƙiƙa Ubangijina yana yalwata arziki ga wanda yaga dama (don gwadawa) yana ƙuntatawa ga wanda yaga dama (don jarrabawa), saidai yawancin mutane (kafiran Makka) basu san wannan ba".
37. Dukiyoyinkuda 'ya'yayenku basu kasance suna kusantaku garemu kusantawa ba, kai dai wađanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagari wadancanenka sakamako ninki nagari na garesu saboda abinda suka aikata, (hasana guda đaya da lada goma da mafi yawa), su suna amintattu (daga mutuwa da waninta) a cikin ɓenayen aljanna, (ba mutuwa badamuwa).
38. Wađannan dasuke ƙoƙari a cikin ɓata ayoyin mu (na kur'ani), suna masu gajiyar da mu kuma da cewa su zasu tsere mana, wađancanen ka suna cikin azaba ababan dauwamarwa
39. Cene, "Ubangijina yana yalwata arziki ga wanda yaga dama (daga bayinsa don gwadawa) yana ƙuntatawa (bayan shin-fiđawa, wato yalwatawa) duk abinda kuka ciyar na koMenene (a cikin aikin alheri) Ubangiji ne zai mayar muku dashi, Shine fiyayyen mai azurtawa.

وَيَوْمَ نَحْشُرُهُمْ جَمِيعًا ثُمَّ نَقُولُ لِلْمَلَٰٓئِكَةِ أَهَٰٓؤُلَآءِ إِيَّاكُمْ كَانُوا
يَعْبُدُونَ ﴿40﴾ قَالُوا سُبْحَٰنَكَ أَنتَ وَلِيُّنَا مِن دُونِهِم بَلْ كَانُوا
يَعْبُدُونَ الْجِنَّ أَكْثَرُهُم بِهِم مُّؤْمِنُونَ ﴿41﴾ فَالْيَوْمَ لَا يَمْلِكُ بَعْضُكُمْ
لِبَعْضٍ نَّفْعًا وَلَا ضَرًّا وَنَقُولُ لِلَّذِينَ ظَلَمُوا ذُوقُوا عَذَابَ
النَّارِ الَّتِي كُنتُم بِهَا تُكَذِّبُونَ ﴿42﴾ وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٍ
قَالُوا مَا هَٰذَا إِلَّا رَجُلٌ يُرِيدُ أَن يَصُدَّكُمْ عَمَّا كَانَ يَعْبُدُ ءَابَآؤُكُمْ
وَقَالُوا مَا هَٰذَا إِلَّا إِفْكٌ مُّفْتَرًى وَقَالَ الَّذِينَ كَفَرُوا لِلْحَقِّ لَمَّا جَآءَهُمْ
إِنْ هَٰذَا إِلَّا سِحْرٌ مُّبِينٌ ﴿43﴾ وَمَا ءَاتَيْنَٰهُم مِّن كُتُبٍ يَدْرُسُونَهَا
وَمَا أَرْسَلْنَا إِلَيْهِمْ قَبْلَكَ مِن نَّذِيرٍ ﴿44﴾ وَكَذَّبَ الَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ
وَمَا بَلَغُوا مِعْشَارَ مَا ءَاتَيْنَٰهُمْ فَكَذَّبُوا رُسُلِي فَكَيْفَ كَانَ نَكِيرِ ﴿45﴾
ربع * قُلْ إِنَّمَا أَعِظُكُم بِوَٰحِدَةٍ أَن تَقُومُوا لِلَّهِ مَثْنَىٰ وَفُرَٰدَىٰ
ثُمَّ تَتَفَكَّرُوا مَا بِصَاحِبِكُم مِّن جِنَّةٍ إِنْ هُوَ
إِلَّا نَذِيرٌ لَّكُم بَيْنَ يَدَيْ عَذَابٍ شَدِيدٍ ﴿46﴾ قُلْ مَا سَأَلْتُكُم
مِّنْ أَجْرٍ فَهُوَ لَكُمْ إِنْ أَجْرِيَ إِلَّا عَلَى اللَّهِ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ
شَيْءٍ شَهِيدٌ ﴿47﴾ قُلْ إِنَّ رَبِّي يَقْذِفُ بِالْحَقِّ عَلَّٰمُ الْغُيُوبِ ﴿48﴾

40. Ka ambaci ranar da muke tara mushurikai baki ɗaya, sannan mu ce da mala'iku, "Shin waɗannan ku suka kasance suna bautawa?".
41. Saisu ce, "Tsarki ya tabbatar maka kaine majibincin mu basu ba,bari sun kasance suna bautawa Shaiɗan ne", (wato suna bin su) yawaicinsu masu bada gaskiya ne da shaiɗanu.
42. Yau ba'alinku bai mallaki ceto ga ba'ali ba, wala azabtawa, Muna faɗa ga waɗannan da suka kafirta, "Ku ɗanɗani azabar Wuta wacce kuka kasance kuna ƙaryatawa da ita".
43. Idan ana karantawan ayoyin Alƙur'ani a garesu halin kasancewarta mabayyaniya (a harshen Annabi Sallallahu alaihi wa sallama) sukAnce , "Wannan bai kasance basai mutumne da yake nufin ya hana ku ga buran abinda iyayenku suka kasance suna bautwa (na daga gumaka)" sukace "Wannan Alƙur'ani bai kasance basai ƙarya ne abin ƙirƙira ga Allah", Waɗanda suka kafirce da alƙur'ani yayin dayazo musu sukace, "wannan ba wani abu bane sai tsafi mabayyani".
44. (Ubangiji yace), "Bamu zo musu da littattafai dasuke karanta ta ba, bamu aiko wani mai gargaɗi gabanka izuwa garesu ba? (To ta ina suka ƙaryata ka?").
45. Waɗanda suke gabansu sun ƙarya ta (Manzanni), waɗannan basu isa la'adar gomanniyan abinda muka basu ba, (wato ushurin ushiri na ƙarfi da tsawon rai da yawan dukiya), sai suka ƙaryata manzannina ((izuwa garesu), Yaya musun da nayi musu (da uƙubaya kasance? (ya afku daidai wa daida).
46. Cene "Ni kawai inayi muku gargaɗi da kalma ɗaya ne (Itace) ku mike tsaye don Allah bibiyu, ɗaiɗai, sannan kuyi tunani, ku sani abokin nan naku ba aljan a gareshi (wato Annabi Sallallahu alaihi wa sallama), shi bai kasance ba, sai mai gargaɗi a gareku nan ga tsakanin gaban azabada tsanani(a lahira inkun sabe shi").
47. Cene dasu ban tambaye ku lada bisa ida aike ba, saboda shi ida aike naku ne, (bazan tambayi lada a kansa ba), ni ladana bai kasance basai ga Allah. Shi Allah mai tsinkayen komai ne, (yasan gaskiyata).
48. Cene (dasu) " Haƙiƙa Ubangijina yana jefa gaskiya (izuwa Annabawa), masanin asirin fake(a cikin sammai da ƙassai).

قُلْ جَآءَ ٱلْحَقُّ وَمَا يُبْدِئُ ٱلْبَٰطِلُ وَمَا يُعِيدُ ﴿49﴾ قُلْ إِن ضَلَلْتُ فَإِنَّمَآ
أَضِلُّ عَلَىٰ نَفْسِى وَإِنِ ٱهْتَدَيْتُ فَبِمَا يُوحِىٓ إِلَىَّ رَبِّىٓ إِنَّهُۥ سَمِيعٌ قَرِيبٌ ﴿50﴾
وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذْ فَزِعُوا۟ فَلَا فَوْتَ وَأُخِذُوا۟ مِن مَّكَانٍ قَرِيبٍ ﴿51﴾ وَقَالُوٓا۟
ءَامَنَّا بِهِۦ وَأَنَّىٰ لَهُمُ ٱلتَّنَاوُشُ مِن مَّكَانٍۭ بَعِيدٍ ﴿52﴾ وَقَدْ كَفَرُوا۟ بِهِۦ مِن قَبْلُ
وَيَقْذِفُونَ بِٱلْغَيْبِ مِن مَّكَانٍۭ بَعِيدٍ ﴿53﴾ وَحِيلَ بَيْنَهُمْ وَبَيْنَ مَا يَشْتَهُونَ
كَمَا فُعِلَ بِأَشْيَاعِهِم مِّن قَبْلُ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ فِى شَكٍّ مُّرِيبٍۭ ﴿54﴾

35 سُورَةُ فَاطِرٍ مَكِّيَّة
وَهِيَ خَمْسٌ وَأَرْبَعُونَ ءَايَةً 45

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ فَاطِرِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ جَاعِلِ ٱلْمَلَٰٓئِكَةِ رُسُلًا أُو۟لِىٓ أَجْنِحَةٍ
مَّثْنَىٰ وَثُلَٰثَ وَرُبَٰعَ يَزِيدُ فِى ٱلْخَلْقِ مَا يَشَآءُ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿1﴾
مَّا يَفْتَحِ ٱللَّهُ لِلنَّاسِ مِن رَّحْمَةٍ فَلَا مُمْسِكَ لَهَا وَمَا يُمْسِكْ فَلَا مُرْسِلَ
لَهُۥ مِنۢ بَعْدِهِۦ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿2﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱذْكُرُوا۟
نِعْمَتَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ هَلْ مِنْ خَٰلِقٍ غَيْرُ ٱللَّهِ يَرْزُقُكُم
مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَأَنَّىٰ تُؤْفَكُونَ ﴿3﴾

49. Cene (dasu), "Musulunci yazo, kafirci baya bayyana baya saura".
50. Cene, "in na ɓata (ga barin gaskiya) to, ina ɓata ne ga kaina kawai, in na shiriya to da abinda Ubangijina ya aiko minine (alƙur'ani da hikima), haƙiƙa Ubangiji mai ji ne (ga mai roƙo) makusanci ne (gareshi).
51. Da kana gani (Ya Muhammadu)! Sallallahu alaika wa sallama), zamanin da suka firgita (zamanin alƙiyama daka ga al'amari mai girma), to ba tsere-wa (daga gare Mu, wato bazasu tsere mana ba) za a danke su daga guri makusanci (Shine kabari wato guri mai nisa ga buran mahallinsa, donsu suna lahira).
52. Sukace, "Mun bada gaskiya da Annabi (Sallallahu alaihi wa sallama, ko da alƙur'ani)", ta ina zasu kamo imani da alƙur'ani a guri mai nisa,(Don sun ,a lahira imani ko muhalinsa duniya!).
53. Haƙiƙa sun kafirtada Allah tun gaba (a nan duniya), suna jifa da gaibu daga guri mai nisa (suna cewa Annabi mai sihiri ne, matsafi ne mawaƙi ne, boka ne alƙur'ani kuma suna cewa tsafi ne, waƙa ce, bokanci ne").
54. An tsare tsakaninsu da abinda suke marmari (na imani) tamfar da aka tsare 'yan'uwansu (a cikin kafarci) tun gaban su saboda sun kasance a cikin kokonto mai afkarwa a cikin tuhuma.

Wannan Surar Faɗiri ce

A Makka aka saukar da ita Aya Arba'in dashida ce (46)

Ina. farawa, dasunan. Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Mimunai a lahira a keɓe

1. Godiya ta tabbata ga Allah mahaliccin sammai da ƙassai (ba tareda misali daya rigaya ba) mai sanya Mala'iku manzanni (izuwa Annabawa), ma'abuta fikafikai bi biyu mabiyanta ma'ukunta mahuɗunta, yana ƙara abinda yaga dama (a cikinta na Mala'ikuda wasunsu).Haƙiƙa shi Ubangiji mai ikone bisa komai.
2. Abinda Allah yayi buɗu dashi ga mutane na rahama (kamar arziki da ruwa) to ba mahani gareta, abinda Allah ya riƙe (na daga wannan) to ba mai saki, ba Allah ba. Shine mabuwayi (a kan al'amarinsa), gwani (cikin aikinsa).
3. Yaku waɗannan mutane (na Makka) ku tuna ni'imar Ubangiji gareku (da zaunar daku ,cikin harami da tare hare -hare ga buran ku). Shin akwai wani mahalicci ba Allah ba, (wanda) yake azurta ku daga sama (da ruwa) daga ƙasa kuma (da tsiri? Babu), ba abin bautawa da gaskiya sai shi, to yaya ake juyar daku ,(ga buran tauhidi tareda furucinku cewa Shine mahalicci mai azurtawa).

ثمن

وَإِن يُكَذِّبُوكَ فَقَدْ كُذِّبَتْ رُسُلٌ مِّن قَبْلِكَ وَإِلَى اللَّهِ تُرْجَعُ الْأُمُورُ ﴿4﴾
* يَا أَيُّهَا النَّاسُ إِنَّ وَعْدَ اللَّهِ حَقٌّ فَلَا تَغُرَّنَّكُمُ الْحَيَاةُ الدُّنْيَا
وَلَا يَغُرَّنَّكُم بِاللَّهِ الْغَرُورُ ﴿5﴾ إِنَّ الشَّيْطَانَ لَكُمْ عَدُوٌّ فَاتَّخِذُوهُ عَدُوًّا
إِنَّمَا يَدْعُو حِزْبَهُ لِيَكُونُوا مِنْ أَصْحَابِ السَّعِيرِ ﴿6﴾ الَّذِينَ كَفَرُوا لَهُمْ
عَذَابٌ شَدِيدٌ وَالَّذِينَ ءَامَنُوا وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ لَهُم مَّغْفِرَةٌ وَأَجْرٌ
كَبِيرٌ ﴿7﴾ أَفَمَن زُيِّنَ لَهُ سُوءُ عَمَلِهِ فَرَءَاهُ حَسَنًا فَإِنَّ اللَّهَ يُضِلُّ مَن
يَشَاءُ وَيَهْدِي مَن يَشَاءُ فَلَا تَذْهَبْ نَفْسُكَ عَلَيْهِمْ حَسَرَاتٍ
إِنَّ اللَّهَ عَلِيمٌ بِمَا يَصْنَعُونَ ﴿8﴾ وَاللَّهُ الَّذِي أَرْسَلَ الرِّيَاحَ فَتُثِيرُ سَحَابًا
فَسُقْنَاهُ إِلَى بَلَدٍ مَّيِّتٍ فَأَحْيَيْنَا بِهِ الْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَا
كَذَلِكَ النُّشُورُ ﴿9﴾ مَن كَانَ يُرِيدُ الْعِزَّةَ فَلِلَّهِ الْعِزَّةُ جَمِيعًا
إِلَيْهِ يَصْعَدُ الْكَلِمُ الطَّيِّبُ وَالْعَمَلُ الصَّالِحُ يَرْفَعُهُ وَالَّذِينَ
يَمْكُرُونَ السَّيِّئَاتِ لَهُمْ عَذَابٌ شَدِيدٌ وَمَكْرُ أُولَئِكَ هُوَ يَبُورُ ﴿10﴾
وَاللَّهُ خَلَقَكُم مِّن تُرَابٍ ثُمَّ مِن نُّطْفَةٍ ثُمَّ جَعَلَكُمْ أَزْوَاجًا
وَمَا تَحْمِلُ مِنْ أُنثَى وَلَا تَضَعُ إِلَّا بِعِلْمِهِ وَمَا يُعَمَّرُ مِن مُّعَمَّرٍ
وَلَا يُنقَصُ مِنْ عُمُرِهِ إِلَّا فِي كِتَابٍ إِنَّ ذَلِكَ عَلَى اللَّهِ يَسِيرٌ ﴿11﴾

4. In sun ƙaryata ka (Ya Annabi Sallallahu alaihi wa sallama a cikin zuwanka da tauhidi da tashin alƙiyama da sauransu) to haƙiƙa an ƙaryata manzanni na daga gabanka (a cikin wannan sai ka daure kamar da suka daure), izuwa Allah al'amura suke komawa (a lahira, haka nan ma a duniya).

(WA'AZI DASHIRYARWA)

5. Yaku waɗannan mutane! haƙiƙa alkawarin Allah (da tashin alƙiyama) gaskiya ne, kada rayuwar duniya ta ruɗe ku, kada Shaiɗan mai ruɗi ya ruɗe ku (da haƙurin Allah da jinkirtawarsa).
6. Haƙiƙa shaiɗanu magauci ne gareku ku riƙe shi magauci, kubi Allah (kar kubi shi) haƙiƙa yana kiran mabiyansa ne donsu kasance 'yan wuta, mai balbalin ƙonawa. Kadaku ,bi shi Shaiɗan shi dai yana jan ƙungiyarsa ne a cikin kafirci kawai, donsu ka-sance daga 'yan wuta.
7. Waɗanda suka kafirta azaba mai tsanani ta tabbata garesu, waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru, gafara da ladasun tabbata garesu, (wannan bayani ga masu dacewa da Shaiɗan da masu saɓa masa ne).

(WAHABIYA ALLAH YAYI MANA MAGANINSU)[1]

8. Shin to wanda aka ƙawata masa mummunan aikinsa (da maguɗantawa, wato ƙawata zahiri kawai), yagan shi kyakkyawa, zai zama kamar wanda Allah ya shiryeshi? (La, bazai zama ba). haƙiƙa Ubangiji yana bad da wanda yaga dama, yana shiryar wanda yaga dama, saboda haka ranka kadata kwaranye don baƙin ciki a garesu, a kan basu .bada gaskiya ba). Haƙiƙa Ubangiji masanine da abinda suke aikatawa, (zaiyi musu sakamako a kansa).
9. Ubangiji Shine wanda yake aiko iskoki su motsa girgije, sai muka kora shi (girgijen) izuwa gari matacce wanda ba tsiri cikinsa, muka raya ƙasa dashi bayan ƙeƙashewarta (Shine muka tsirar da hatsi da ciyawar dabbobi dashi ruwan nan, kamar haka tashin alƙiyama yake, (haka nan tashin mutane da raya su yake).
10. Wanda yake nufin izza to izzata Allah ce baki ɗaya (a duniya da lahira, baza a same ta basai daga gareshi), izuwa gareShine kalmomi daɗaɗa suke hauhawa (da iliminsa, wato Shine LA ILAHA ILLALLAHU da makamancinta). Aiki nagari Allah yana karbar sa, waɗanda suke makirci, miyagun aikace-aikace (ga Annabi Sallallahu alaihi wa sallama a gidan shawara na daga tsare shi, ko kashe shi, ko fishshe shi), azaba mai tsanani ta tabbata garesu, makircin wancanenka Shine wanda yake halakakke.

(AYOYI MASU SHIRYARWA BISA IKON ALLAH DA TASHIN ALƘIYAMA)

11. Ubangiji Shine ya halicceku daga turɓaya, (wato ya halicci ubanku Annabi Adamu daga Ita), sannan ya halicci zurriya tasa daga digon maniyi, sannan yasanya ku mazaje da mataye, ba wata mace daza tayi ciki wala ta haihu saida sanin Allah, baza a tsawaita daga wanda aka tsawaita ransa ba, ko a tauye daga abin tsawaita ran nan nasa ba, face yana cikin littafi (na Lauhul Mahfuzu), Haƙiƙa wancanenka mai sauƙine bisa Ubangiji.

1) wannan ya sauka ne a cikin Abu Jahil da waninsa na daga Mushirkan Makka kamar Asi dan Wa'ily da Aswadu dan Muddalibu da Ukbatu Abu Mu'aidin kuma Ance wannan aya ta sauka ne a cikin khawarijawa, wato makangara waɗanda suke jirkita tawilin Alƙur'ani da Hadisi, suke halatta jinin Musulmi da dukiyoyin-su, tamfar da yake abin gani da waninsu, mak-amantansu sune wadansu jama'a a ƙasar Hijas ana ce dasu Wahabiya, suna zaton su a kan wani abu suke, na'am sune ainihin makaryata, shaiɗan ya rinjaye kansu, ya mantar dasu an-baton Allah. Wadancanenka sune rundunar shaiɗan, na'am, haƙiƙa rundunar Shaiɗan sune taɓaɓɓu, muna rokon Allah Ta'ala ya tumbuke asalinsu, Amin-sawi-: In Allah yasan bazasu shiriya ba, in ko Allah yasan zasu shiriya, to Allah ya shirye mu da mu dasu baki ɗaya amin. -Sanajiy-.

وَمَا يَسْتَوِے اِ۬لْبَحْرَانِۖ هَٰذَا عَذْبٞ فُرَاتٞ سَآئِغٞ شَرَابُهُۥ وَهَٰذَا
مِلْحٌ اُجَاجٞۖ وَمِن كُلّٖ تَأْكُلُونَ لَحْماً طَرِيّاٗ وَتَسْتَخْرِجُونَ حِلْيَةٗ
تَلْبَسُونَهَاۖ وَتَرَى اَ۬لْفُلْكَ فِيهِ مَوَاخِرَ لِتَبْتَغُواْ مِن فَضْلِهِۦ
وَلَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَۖ (12) يُولِجُ اُ۬ليْلَ فِے اِ۬لنَّهَارِ وَيُولِجُ اُ۬لنَّهَارَ
فِے اِ۬ليْلِۖ وَسَخَّرَ اَ۬لشَّمْسَ وَالْقَمَرَۖ كُلّٞ يَجْرِے لِأَجَلٖ مُّسَمّيۖ
ذَٰلِكُمُ اُ۬للَّهُ رَبُّكُمْ لَهُ اُ۬لْمُلْكُۖ وَالذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِهِۦ
مَا يَمْلِكُونَ مِن قِطْمِيرٍۖ (13) إِن تَدْعُوهُمْ لَا يَسْمَعُواْ دُعَآءَكُمْ
وَلَوْ سَمِعُواْ مَا اَ۪سْتَجَابُواْ لَكُمْۖ وَيَوْمَ اَ۬لْقِيَٰمَةِ يَكْفُرُونَ
بِشِرْكِكُمْۖ وَلَا يُنَبِّئُكَ مِثْلُ خَبِيرٖۖ (14) ۞ يَٰأَيُّهَا اَ۬لنَّاسُ أَنتُمُ اُ۬لْفُقَرَآءُ ربع
إِلَى اَ۬للَّهِۖ وَاللَّهُ هُوَ اَ۬لْغَنِيُّ اُ۬لْحَمِيدُۖ (15) إِن يَّشَأْ يُذْهِبْكُمْ
وَيَأْتِ بِخَلْقٖ جَدِيدٖۖ (16) وَمَا ذَٰلِكَ عَلَى اَ۬للَّهِ بِعَزِيزٖۖ (17)
وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٞ وِزْرَ أُخْرَيٰۖ وَإِن تَدْعُ مُثْقَلَةٌ اِلَيٰ حِمْلِهَا
لَا يُحْمَلْ مِنْهُ شَےْءٞ وَلَوْ كَانَ ذَا قُرْبَيٰٓۖ إِنَّمَا تُنذِرُ اُ۬لذِينَ
يَخْشَوْنَ رَبَّهُم بِالْغَيْبِ وَأَقَامُواْ اُ۬لصَّلَوٰةَۖ وَمَن
تَزَكَّيٰ فَإِنَّمَا يَتَزَكَّيٰ لِنَفْسِهِۦۖ وَإِلَى اَ۬للَّهِ اِ۬لْمَصِيرُۖ (18)

12. Kogi biyu bazasuyidaidai ba, wannan mai dadi ne makwararin shan sa, wannan mai zartsi ne mai tsananiri zartsi, daga kowanne daga cikinsu kuna cin nama ɗanye, (Shine kifi) kuna fitarwa da kayan ado da kuke ɗaurata, (lu'u-lu'u ke nan, da murjanu), kana ganin jirage a cikin kowanne daga cikinsu suna keta ruwa', (da gudunta cikinsa, tana mai gabatowa ko tana mai bada baya da iska guda ɗaya), domin ku nema daga falalar Allah (ta wajen ci-niki) don ku godewa Allah (bisa wannan).
13. Ubangiji yana shigar da dare cikin rana, yana shigar da rana cikin dare, (yakuru), ya hore rana da wata, kowanne daga cikinsu yana gudana (cikin falakinsa) izuwa ajali abin ambato (ranar alƙiyama), wancanenku Allah ne Ubangijinku, mulki na gareshi, waɗanda kuke bautawa ba Allah ba, (na gumaka), basu mallaki tantanin dan balle ba.
14. Inkun kirasu bazasuji kiran ku ba, in da ma zasuji, taƙdiran bazasu amsa muku ba, ranar alƙiyama zasu kafirtada tara su da kukayi da Allah, (su kubuta daga gareku, da kuma bautar da kuke musu) ba mai baka labarin halin duniya da lahira irin masanin asirin fake.

(WA'AZI DASHIRYARWA)

15. Yaku waɗannan mutane, kune haƙiƙanin mabuƙata izuwa Allah (ta'ala) a kowane hali. Ubangiji Shine mawadaci (ga buran halitta tasa), abin godewa cikin (aikinsa gami dasu).
16. In yaga dama saiya tafi da ku, yazoda halitta sabuwa.
17. Wancanenka bai kasance mai wuya ba, gurin Allah (ta'ala).
18. Wata kai bazata ɗauki zunubin wata kai ba, idan wata kai abar nauyayawa da zunubi ta kira wani domin ya ɗauki sashin zunubin, baza a ɗauki komai daga gareshi ba koda abin kiran nan ya kasance abin zumunci ne, (kamar ubako ɗa, haka Allah ya hukunta a kowane ɓari, wato abindauka babbada abin ɗauka ƙarami, babbakamar sammai, ƙarami kamar ƙwayar komayya), kai dai kana gargaɗi ne ga waɗanda suke tsoron Ubangijinsu a fake,suka dbrar da sallah. Wanda ya tsarkake (daga shirka da waninsa), ya tsarkake ne don kansa, izuwa Allah kowa zai koma (ya ramawa kowa da abinda ya aikata).

وَمَا يَسْتَوِے اِ۬لْأَعْمَيٰ وَالْبَصِيرُ ﴿19﴾ وَلَا اَ۬لظُّلُمَٰتُ وَلَا اَ۬لنُّورُ ﴿20﴾
وَلَا اَ۬لظِّلُّ وَلَا اَ۬لْحَرُورُ ﴿21﴾ وَمَا يَسْتَوِے اِ۬لْأَحْيَآءُ وَلَا اَ۬لْأَمْوَٰتُ
إِنَّ اَ۬للَّهَ يُسْمِعُ مَنْ يَّشَآءُ وَمَا أَنتَ بِمُسْمِعٍ مَّن فِے اِ۬لْقُبُورِ ﴿22﴾
إِنْ أَنتَ إِلَّا نَذِيرٌ ﴿23﴾ إِنَّا أَرْسَلْنَٰكَ بِالْحَقِّ بَشِيراً وَنَذِيراً
وَإِن مِّنْ اُمَّةٍ إِلَّا خَلَا فِيهَا نَذِيرٌ ﴿24﴾ وَإِن يُّكَذِّبُوكَ فَقَدْ كَذَّبَ
اَ۬لذِينَ مِن قَبْلِهِمْ جَآءَتْهُمْ رُسُلُهُم بِالْبَيِّنَٰتِ وَبِالزُّبُرِ
وَبِالْكِتَٰبِ اِ۬لْمُنِيرِ ﴿25﴾ ثُمَّ أَخَذتُّ اُ۬لذِينَ كَفَرُواْ فَكَيْفَ
كَانَ نَكِيرِ ﴿26﴾ أَلَمْ تَرَ أَنَّ اَ۬للَّهَ أَنزَلَ مِنَ اَ۬لسَّمَآءِ مَآءً
فَأَخْرَجْنَا بِهِۦ ثَمَرَٰتٍ مُّخْتَلِفاً أَلْوَٰنُهَا وَمِنَ اَ۬لْجِبَالِ جُدَدُۢ بِيضٌ
وَحُمْرٌ مُّخْتَلِفٌ أَلْوَٰنُهَا وَغَرَابِيبُ سُودٌ ﴿27﴾ وَمِنَ اَ۬لنَّاسِ
وَالدَّوَآبِّ وَالْأَنْعَٰمِ مُخْتَلِفٌ أَلْوَٰنُهُۥ كَذَٰلِكَ إِنَّمَا يَخْشَى
اَ۬للَّهَ مِنْ عِبَادِهِ اِ۬لْعُلَمَٰٓؤُاْ إِنَّ اَ۬للَّهَ عَزِيزٌ غَفُورٌ ﴿28﴾
إِنَّ اَ۬لذِينَ يَتْلُونَ كِتَٰبَ اَ۬للَّهِ وَأَقَامُواْ اُ۬لصَّلَوٰةَ وَأَنفَقُواْ
مِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ سِرّاً وَعَلَانِيَةً يَرْجُونَ تِجَٰرَةً لَّن تَبُورَ ﴿29﴾
لِيُوَفِّيَهُمُۥٓ أُجُورَهُمْ وَيَزِيدَهُم مِّن فَضْلِهِۦٓ إِنَّهُۥ غَفُورٌ شَكُورٌ ﴿30﴾

19. Makaho da mai gani (wato kafiri da mumini) bazasuyidaidai ba.
20. Wala duffai (wato kafirci) wala haske (wato imani).
21. Wala inuwa (wato aljanna) wala zafi (wato wuta).
22. rayayyu bazasuyidaidai ba, (wato muminai) wala matattu (wato kafirai), haƙiƙa Ubangiji yana jiyar da wanda yaga da-mar (shiriyarsa, saiya amsa da imani) kai baka kasance mai jiyar da waɗanda suke cikin .ƙaburbura ba, (wato kafurai bare su amsa).
23. Kai baka kasance basai mai gargaɗi (garesu).
24. Haƙiƙa mun aiko ka da gaskiya (wato shiriya) kana mai albishir (ga wanda ya amsa), kana gargaɗi (ga wanda bai amsa ba), babu daga al'umma face niai gargaɗi ya 'vuce cikinta (Shine Annabi mai gargaɗi).
25. In sun ƙaryata ka (wato mutan Makka) haƙiƙa kuma an karyatasu manzanni gaban zamaninsu sun zo musu da hujjoji (wato mu'ujuzai) sun zoda littafi mai haske (Shine Attaura da Injila, sai ka dauretamfar da suka daure).
26. Sannan na kama waɗanda suka kafirta (saboda ƙaryatawar nan tasu), Yaya inkarin da nayi musu na ukuba? (Ya afku gurin afkuwarsa).

(DARAJOJIN MASU TSORON ALLAH)

27. Shin baka sani ba haƙiƙa Ubangiji ya saukar da ruwa daga sama? Muka fitar da 'ya'yan it-atuwa da wannan ruwa, wanda yake launinta dabam-dabam, (kamar kore da ja dayarani da waninsu), akwai ta-farku daga duwarwatsu farare da jajaye dayaranai, masu sabawar launonintada bakakekirin.
28. Akwai daga mutane da dabbobi da shanu da rakuma da tumakai, mai sassabawar launinsa kamar wancanenka sabawar 'ya'yan it-atuwa da duwarwatsu, Malamai ne kaɗai suke jin tsoron Allah daga cikin bayinsa,(sabanin jahi-lai kamar kafiran Makka) haƙiƙa Ubangiji mabuwayi ne (cikin mulkinsa) mai gafara ne (ga zunuban bayinsa muninai).
29. Haƙiƙa waɗanda suke karantaw-an littafin Allah suka dauwama kan tsaida sallah (tareda hakkokinta), suka ciyar daga abinda muka azurta musu na asirce da bayyane, (Zakka ko waninta), suna jin tsoron ciniki wacce bata halaka ba.
30. Donya cika musu ladansu, ya kara musu daga falalarsa, haƙiƙa shi mai gafara ne (ga zunubansu) mai godiya ne (ga da'arsu).

ثمن

* والذي أوحينا إليك من الكتاب هو الحق مصدقا لما
بين يديه إن الله بعباده لخبير بصير 31 ثم أورثنا
الكتاب الذين اصطفينا من عبادنا فمنهم ظالم لنفسه
ومنهم مقتصد ومنهم سابق بالخيرات بإذن الله
ذلك هو الفضل الكبير 32 جنات عدن يدخلونها يحلون
فيها من أساور من ذهب ولؤلؤا ولباسهم فيها حرير 33
وقالوا الحمد لله الذي أذهب عنا الحزن إن ربنا
لغفور شكور 34 الذي أحلنا دار المقامة من فضله
لا يمسنا فيها نصب ولا يمسنا فيها لغوب 35 والذين
كفروا لهم نار جهنم لا يقضى عليهم فيموتوا ولا يخفف
عنهم من عذابها كذلك نجزي كل كفور 36
وهم يصطرخون فيها ربنا أخرجنا نعمل صالحا غير الذي كنا
نعمل أولم نعمركم ما يتذكر فيه من تذكر وجاءكم
النذير فذوقوا فما للظالمين من نصير 37 إن الله
عالم غيب السماوات والأرض إنه عليم بذات الصدور 38

(ALƘUR'AN DA WAƊANDA SUKA GASGATA DASHI DA WAƊANDA SUKA KAFIRCE DASHI)

31. Abinda muka aiko gareka na daga Alƙur'ani Shine gaskiya, mai gasgatawa ga abinda yake gabansa na daga littattafai, haƙiƙa Ubangiji lallai masanin asirin fake ne na bayinsa (daga abinda yake bayyane, da ɓoyayye).

(GIRMAN AL'UMAR MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAMA)

32. Sannan muka gadawa waɗanda muka zaɓe su daga bayin mu (wato muka gada musu) Alƙur'ani (sune al'umir-arka), to akwai daga garesu, wanda yake mai zaluntar kansa, (da takaitawa a cikin aiki da Alƙur'ani), akwai daga garesu mai tsaƙaitawa (yana aiki dashi a cikin mafi rinjayen lokatai), akwai daga garesu mai tsere da alheri, (ya tara ilimi izuwa aiki da shi, da shiryarwa ga al'umma), da izinin Ubangiji. Wancanenka (gada musu alƙur'ani), Shine falala mai girtna.
33. (Waɗancanenka) aljannatai ne na zama, waɗanda zasu shigeta, anayi musu ƙawa da kwandagai na zinare, kuma anayi musu Kawa da lu'ulu'i, (abindanfarawa da zinare), abindaurawarsu cikinsa alharini ne.
34. Sukace, "Alhamdu lillahi, godiya ta tabbata ga Ubangiji wanda ya tafiyar da dukkan baƙin ciki daga garemu, haƙiƙa Ubangiji mai yawan gafara ne (ga zu-nubai), mai yawan godiya ne (ga aiyukan da'a). \
35. Wanda ya saukar da mu gidan dauwama daga falala tasa, babu wahala ko gajiyawa dazai same mu a cikinta.
36. Waɗanda suka kafirta kuwa wutar jahannama ta tabbata garesu, baza ayi hukunci garesu da mutuwa ba, barc su mutu (su huta), baza a sauwaƙe wani abu na azabar ta ga buran su ba, (kiftawar ido), irin yadda mukayi musu sakamako, muke sakawa dukkan kafiri.
37. Su suna kumruwa a cikinta, (suna cewa) "Ya Ubangijinmu! fitar da mu daga cikinta, mu yi aiki nagari, ba wanda muka ka-sance muna aikatawa ba" (Sai a ce dasu), Shin bamu rayaku gwargwadon lokaci da wandazai gargadu zai gargaɗu a cikinsa, kuma mai gargaɗi bai zo muku bane? (Shine Manzo, baku amsa masa ba?) To ku ɗanɗani kuɗar ku, azzalumai. Basu da mai ije musu azbar Ubangiji.
38. Haƙiƙa Ubangiji masanin asirin fake ne a cikin sammai da ƙassai, shi Ubangiji masanine da abinda yake cikin zukatan bayi, (saninsa da abinda ya bayyana min babi aula ne).

هُوَ ٱلَّذِے جَعَلَكُمْ خَلَٰٓئِفَ فِے ٱلْأَرْضِ فَمَن كَفَرَ فَعَلَيْهِ كُفْرُهُۥ وَلَا يَزِيدُ ٱلْكَٰفِرِينَ
كُفْرُهُمْ عِندَ رَبِّهِمْ إِلَّا مَقْتاً وَلَا يَزِيدُ ٱلْكَٰفِرِينَ كُفْرُهُمْ إِلَّا خَسَاراً ﴿39﴾
ربع
* قُلْ أَرَآيْتُمْ شُرَكَآءَكُمُ ٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَرُونِے مَاذَا خَلَقُواْ مِنَ
ٱلْأَرْضِ أَمْ لَهُمْ شِرْكٌ فِے ٱلسَّمَٰوَٰتِ أَمْ ءَاتَيْنَٰهُمْ كِتَٰباً فَهُمْ عَلَىٰ بَيِّنَٰتٍ مِّنْهُ
بَلْ إِن يَعِدُ ٱلظَّٰلِمُونَ بَعْضُهُم بَعْضاً إِلَّا غُرُوراً ﴿40﴾ إِنَّ ٱللَّهَ يُمْسِكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ أَن تَزُولَا وَلَئِن زَالَتَا إِنْ أَمْسَكَهُمَا مِنْ أَحَدٍ مِّنۢ بَعْدِهِۦ
إِنَّهُۥ كَانَ حَلِيماً غَفُوراً ﴿41﴾ وَأَقْسَمُواْ بِٱللَّهِ جَهْدَ أَيْمَٰنِهِمْ لَئِن جَآءَهُمْ نَذِيرٌ
لَّيَكُونُنَّ أَهْدَىٰ مِنْ إِحْدَى ٱلْأُمَمِ فَلَمَّا جَآءَهُمْ نَذِيرٌ مَّا زَادَهُمْ إِلَّا نُفُوراً ﴿42﴾
إِسْتِكْبَاراً فِے ٱلْأَرْضِ وَمَكْرَ ٱلسَّيِّئِ وَلَا يَحِيقُ ٱلْمَكْرُ ٱلسَّيِّئُ إِلَّا بِأَهْلِهِۦ
فَهَلْ يَنظُرُونَ إِلَّا سُنَّتَ ٱلْأَوَّلِينَ فَلَن تَجِدَ لِسُنَّتِ ٱللَّهِ تَبْدِيلاً
وَلَن تَجِدَ لِسُنَّتِ ٱللَّهِ تَحْوِيلاً ﴿43﴾ أَوَلَمْ يَسِيرُواْ فِے ٱلْأَرْضِ فَيَنظُرُواْ
كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ وَكَانُوٓاْ أَشَدَّ مِنْهُمْ قُوَّةً
وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُعْجِزَهُۥ مِن شَےْءٍ فِے ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِے ٱلْأَرْضِ
إِنَّهُۥ كَانَ عَلِيماً قَدِيراً ﴿44﴾ وَلَوْ يُؤَاخِذُ ٱللَّهُ ٱلنَّاسَ بِمَا كَسَبُواْ مَا تَرَكَ عَلَىٰ ظَهْرِهَا
مِن دَآبَّةٍ وَلَٰكِن يُؤَخِّرُهُمْ إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى فَإِذَا جَآءَ أَجَلُهُمْ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِعِبَادِهِۦ بَصِيراً ﴿45﴾

39. Shine wanda yasanya ku mana ya juna, (wato ba'alinku yana mayewa ba'ali), to duka wanda ya kafirta (daga cikinku) to kafircinsa na gareshi, (wato zai ɗanɗani ƙudarsa ta kafircinsa). Kafirai Kafircinsu baya dada musu komai sai harzuka nan ga Ubangijinsu, kafirai, kafircinsu baya dada musu komai saitabewa (a lahira).
40. Cene, "ku nuna mini gumakan ku waɗanda kuke riya mini ba Allah ba, (waɗanda kuke riyawar cewa su sharikan Ubangiji ne), ku bani labarin me suka halitta a cikin ƙasa, ko ko suna da tarayya ne tareda Allah a cikin halittar sammai? ko mun basu littafi ne? To su suna kan hujja daga gareshi (cewa suna kan shirka tareda ni?") Bari Sudai kafirai ba'alinsu ba yayiwa ba'alinsu alkawari sai ruɗi (da faɗinsu gumaka tana cetonsu).
41. Haƙiƙa Ubangiji ya riƙe sammai da ƙassaiya hana su daga gushewa (daga buran indasuke), Wallahi in suka kau ba wani mutum dazai riƙe su, haƙiƙa Ubangiji ya tabbata mai jinkirin azaba (ga waɗanda suka cancanta), mai gafara (ga abin suka aikata).
42. Kafiran Makkah sun rantse da Allah iyakacin KoKarinsu a rantsuwa, Wallahi in mai gargaɗi yazo musu zasu ƙasance daga mafiya shiriya daga dayan al'umma, (wato yahudu da Nasara da waninsu), yayin da mai gargaɗi yazo musu (Shine Annabi Sallallahu alaihi wa sallama) zuwan nasa bai ƙara musu komai basai burɗaɗa ga buran shiriya.
43. Don ginnan kai a bayan ƙasa (ga buran imani) da makirci mummuna, (Shine shirka da waninsa), saidai makirci mum-muna baya kewaye wa sai ga ma'abotansa, basa sauram ko-mai sai al'adar mutanen farko (na dagayi musu azaba don ƙaryata manzanni), bazaka sami sakewa ga sunnar Allah ba [1].
44. Bazaka sami musanyawa ga al'adar Ubangiji ba har abada, (ba a baddala azaban nan ba, bakuma za a aikawa wanda bai cancanceta ba)[1]. Shin basuyitafiya bane a bayan ƙasa? Yaya ƙarshen waɗanda suke gabansu ya kasance? Sun kasance mafiya tsananin ƙarfi daga garesu, (sai Allah ya halakar dasu, saboda sun ƙaryata Annabawansu), Ubangiji bai zamo wani abu yagajiyar dashi a cikin sammai da ƙassai ba, haƙiƙa Ubangiji masanine (da abubuwa dukkanta), mai ikone (a kanta).
45. Da Allah yana riƙon abinda mutane suka aikata (na daga sabanni), bazai bar wata dabba mai rarrafe a bayan ƙasa ba, kai dai yana jinkirta musune izuwa lokaci abin ambato, idan ajalinsu yazo, haƙiƙa Ubangiji ya tabbata masani da bayinsa.

1) Wato tabdili kamar za ayi masa azabada kishirwa, a musanya ayi masa azabada dauri. -Sanajiy
2). Tahwili- baza a kai ta ga wanda bai cancance-ta ba, kamar an rubuta za ayi wa Amru a musanya a kai wa Zaidu. masalan. -Sanajiye-

36 سُورَةُ يسٓ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ ثِنْتَانِ وَثَمَانُونَ ءَايَةً 82

ثمن

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

* يسٓ وَالْقُرْءَانِ الْحَكِيمِ (1) إِنَّكَ لَمِنَ الْمُرْسَلِينَ (2) عَلَيٰ
صِرَاطٍ مُّسْتَقِيمٍ (3) تَنزِيلَ الْعَزِيزِ الرَّحِيمِ (4) لِتُنذِرَ
قَوْماً مَّا أُنذِرَ ءَابَآؤُهُمْ فَهُمْ غَافِلُونَ (5) لَقَدْ حَقَّ الْقَوْلُ
عَلَيٰ أَكْثَرِهِمْ فَهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ (6) إِنَّا جَعَلْنَا فِي أَعْنَاقِهِمْ
أَغْلَالاً فَهْيَ إِلَى الْأَذْقَانِ فَهُم مُّقْمَحُونَ (7)
وَجَعَلْنَا مِنۢ بَيْنِ أَيْدِيهِمْ سُدّاً وَمِنْ خَلْفِهِمْ سُدّاً
فَأَغْشَيْنَاهُمْ فَهُمْ لَا يُبْصِرُونَ (8) وَسَوَآءٌ عَلَيْهِمْ ءَآنذَرْتَهُمْ
أَمْ لَمْ تُنذِرْهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ (9) إِنَّمَا تُنذِرُ مَنِ اتَّبَعَ الذِّكْرَ
وَخَشِيَ الرَّحْمَٰنَ بِالْغَيْبِ فَبَشِّرْهُ بِمَغْفِرَةٍ وَأَجْرٍ كَرِيمٍ (10)
إِنَّا نَحْنُ نُحْيِ الْمَوْتَيٰ وَنَكْتُبُ مَا قَدَّمُواْ وَءَاثَارَهُمْ
وَكُلَّ شَيْءٍ اَحْصَيْنَاهُ فِي إِمَامٍ مُّبِينٍ (11) وَاضْرِبْ
لَهُم مَّثَلاً أَصْحَٰبَ الْقَرْيَةِ إِذْ جَآءَهَا الْمُرْسَلُونَ (12)

Wannan Surata Yasin ce
A Makka aka saukar da ita Aya tamanin da biyuce (82)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talakai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a lahira a keɓe

(Wannan Sura, Sura ce mai falala da yawa, ta tabbatar da tashin alƙiyama, ta ƙunshi sirrin alƙur'an da Ma'aikin Allah (sallallahu alaihi wa sallama) ta kan harufan Ya-sin da tabbatar da tashin Alƙiyama da misalce-misalce da ambaton ƙassoshi da kulawa da mana kan Allah kasantattu da munaƙasha ga kafirai a cikin shashin ƙudure-ƙudurensu, da aikace-aikacensu, da labaran alƙiyama da tauhidi, da tashin Alƙiyama tareda kafa dalili na ganin ido a kan tashin alƙiyama, da ƙaryata rikice-rikicen mushurukai dayanke hujjojinsu, duk waɗannan suna taruwa su kai taimako a kan zukata dataƙe ƙashe, kuma tareda falala da asirai iri-iri har dai ta kai ga cewa Annabi yace, "Itace Zuciyar Alƙur'an", kamar yadda Sawi ya ruwaita)

1. Allahu a'alamu bi muradihi bi zalika, ubangiji ya rantse da alƙur'ani mai hikima, (abin ingantawa da tsari mai ban mana ki da mai ƙaye).
2. Haƙiƙa kai (Ya Annabi Sallallahu alaihi wa sallama) Lallai kai kana daga cikin manzannin Ubangiji.
3. Kana kan tafarki madaidaici (tafarkin Annabawa gabanka, wato tauhidi dashiryarwa. Wannan raddi ne ga faɗin kafirai dasuke cewa "Kai ba manzo bane kai").
4. Alƙur'ani saukarwar sarki ne mabuwayi (cikin mulkinsa), iriai jinƙai (ga halittarsa).
5. Domin ka gargaɗar da mutane, waɗanda ba a yiwa iyayensu gargaɗi ba (a zamanin fatara), saboda haka su mutanen nan marafkana ne (ga buran shi riya).
6. Haƙiƙa magana da azabata waja-ba a bisa yawaicinsu sabock haka su bazasu bada gaskiyi ba.
7. Haƙiƙa mu mun sanya ƙuƙumai a cikin wuyayinsu, (wato Shine a tara hannuwansu izuwa gareta, domin ita ankwa tana tara hannuwa izuwa wuya), tosu masu ɗaukaka kawukansu ne, (basu da ikon saukar da ita, wato wannan misali ne aka saka a kan cewa su bazasu sunkuya kawukansu gashi ba).
8. Mun sanya toshiya a tsakanir hannayensu da toshiya a bayansu, muka lullube su (wato muka dimde idanunsu), su bazasu ga gaskiya ba.
9. Gargaɗinka da rashin gargaɗinka duk ɗaya ne a garesu, bazasu bada gaskiya ba.
10. Dahir dai, kana gargaɗi ne ga wanda yabi alƙur'ani, yaji tsoron Ubangiji mai yawan jinƙai, a fake ba tare dayagan shi ba, to yi masa albishir da gafara da lada mai girma (Shine gidan Aljanna).
11. Haƙiƙa Mu mune masu raya matattu (ran tshin alƙiyama), muna rubuta abinda suka gabatar (na hairi ko sharri a cikin Lauhil gabatar (na hairi ko sharri a cikin Lauhil Mahfuzu, don a yimasu sakamako a kansa), da gurabansu, (wato muna rubuta abubuwan da suka gadar dashi bayansu, kamar ilimi da suka sanar dashi, ko littafi da sukayi talifinsa. ko dabino da suka dasa shi, ko waƙafi da sukayi hubisinsa), kuma kowane abu mun kiyaya shi a cikin limami abin bayyanawa, (Shine Lauhil Mahfuzu).
12. Ka sanya maisali na Ashabil ƙaryati a garesu, (Anɗaƙiya[1] zamanin da jakadun Annabi Isa sukazo mata.

1) Gari ne a ƙasar mai katanga babba, ta duwar-watsu, tana tsakanin dutse biyar kewayenta mil goma sha biyu (12). -Sanajiy

إِذْ أَرْسَلْنَا إِلَيْهِمُ اثْنَيْنِ فَكَذَّبُوهُمَا فَعَزَّزْنَا بِثَالِثٍ
فَقَالُوا إِنَّا إِلَيْكُم مُّرْسَلُونَ ﴿13﴾ قَالُوا مَا أَنتُمْ إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُنَا
وَمَا أَنزَلَ الرَّحْمَٰنُ مِن شَيْءٍ إِنْ أَنتُمْ إِلَّا تَكْذِبُونَ ﴿14﴾
قَالُوا رَبُّنَا يَعْلَمُ إِنَّا إِلَيْكُمْ لَمُرْسَلُونَ ﴿15﴾
وَمَا عَلَيْنَا إِلَّا الْبَلَاغُ الْمُبِينُ ﴿16﴾ قَالُوا إِنَّا
تَطَيَّرْنَا بِكُمْ لَئِن لَّمْ تَنتَهُوا لَنَرْجُمَنَّكُمْ وَلَيَمَسَّنَّكُم
مِّنَّا عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿17﴾ قَالُوا طَائِرُكُم مَّعَكُمْ أَئِن
ذُكِّرْتُم بَلْ أَنتُمْ قَوْمٌ مُّسْرِفُونَ ﴿18﴾ وَجَاءَ مِنْ
أَقْصَا الْمَدِينَةِ رَجُلٌ يَسْعَىٰ قَالَ يَا قَوْمِ اتَّبِعُوا الْمُرْسَلِينَ ﴿19﴾
اتَّبِعُوا مَن لَّا يَسْأَلُكُمْ أَجْرًا وَهُم مُّهْتَدُونَ ﴿20﴾
وَمَا لِيَ لَا أَعْبُدُ الَّذِي فَطَرَنِي وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿21﴾ ءَأَتَّخِذُ
مِن دُونِهِ آلِهَةً إِن يُرِدْنِ الرَّحْمَٰنُ بِضُرٍّ
لَّا تُغْنِ عَنِّي شَفَاعَتُهُمْ شَيْئًا وَلَا يُنقِذُونِ ﴿22﴾ إِنِّي إِذًا
لَّفِي ضَلَالٍ مُّبِينٍ ﴿23﴾ إِنِّي آمَنتُ بِرَبِّكُمْ فَاسْمَعُونِ ﴿24﴾ قِيلَ ادْخُلِ الْجَنَّةَ
قَالَ يَا لَيْتَ قَوْمِي يَعْلَمُونَ ﴿25﴾ بِمَا غَفَرَ لِي رَبِّي وَجَعَلَنِي مِنَ الْمُكْرَمِينَ ﴿26﴾

13. Yayin da muka aiko mutum biyu izuwa garesu suka ƙaryata su, muka ƙarfafa biyun nan dana uku, sai sukace " Haƙiƙa mu jakadu ne izuwa gareku".

14. Sai sukace, "Ku baku kasance ba, sai mutane kamar mu, Ubangiji Arrahamanu bai saukar da komai ba, ku dai ƙaryakuke".

15. Jakadun Annabi Isa sukace, "Ubangijinmu yasan cewa, haƙiƙa mu jakadu ne izuwa gareku".

16. "Ba wani abu a kanmu sai iyad da aike mabayyani (da dalilai mabayyana kamar warkar da wanda aka haifa da makantada maras lafiya da raya matacce").

17. Sukace, " Haƙiƙa mu munyi shi'umi da ku, (saboda ruwa ya ɗauke, saboda shi'uminku), Wallahi inbaku hanu ba, ma jajjefe kuda duwarwatsu. Azaba mai raɗaɗi zata samu gareku daga garemu"

18. Sukace "Shu'uminku yana taredaku ,(saboda kafircinku). Shin kwayi shu'umi ku kafirta don an yi muku gargaɗi? Bari! Ku dai mutane ne masu shishshigi, (wato ƙetare iyaka saboda mushirukancin ku").

19. Wani mutum yazo daga mafi nisan Madina (Shine Habibu Najjaru, ya kasance ya bada gaskiya da jakadun Annabi Isa, unguwarsu tana mafi nisa daga garin, yazo) yana gaggawa (wato aguje yayin dayaji ƙaryatawan jakadun) yace, "Yaku mutanena kubi waɗannan manzanni (jakadun Annabi Isa).

20. "Kubi wanda bazai tambaye ku lada (a kan aikinsa) ba alhali suna shiryayyu".

21. (Sai akace dashi, "Kai a kan addininsu kake?" Sai yace), "Me ke gareni wanda bazan bautawa wanda ya halicce ni ba, (ai ba mai hana ni daga bautarsa). Izuwa gareshi zayi muku sakamako, bayan kafircinku).

22. Yaya zan riƙi iyayen giji ba Allah ba?, (wato gumaka), in Ubangiji Arrahamanu ya nufe ni da ciwo cetonsu (wacce kul riya), baza tayi min anfani komai ba, su kuma bazasu tsamo ni ba.

23. Haƙiƙa ni a yayin nan, lallai ina cikin ɓata mabayyani.

24. Haƙiƙa ni na bada gaskiya da Ubangijinku ku saurari (maganata, suka jefe shiya mutu).

25. Akace dashi (bayan mutuwarsa) "shiga aljanna". (Ance ya shigetada ransa), yace, "woho ho! daya-ka-ce mutanena sun sani.

26 . "Gafarar da Ubangijina yayi mini yasanya ni cikin ababan girmama wa".

حزب

۞ وَمَا أَنزَلْنَا عَلَىٰ قَوْمِهِۦ مِنۢ بَعْدِهِۦ مِن جُندٍ مِّنَ السَّمَآءِ
وَمَا كُنَّا مُنزِلِينَ ﴿27﴾ إِن كَانَتْ إِلَّا صَيْحَةً وَاحِدَةً فَإِذَا هُمْ
خَامِدُونَ ﴿28﴾ يَا حَسْرَةً عَلَى الْعِبَادِ مَا يَأْتِيهِم مِّن رَّسُولٍ
إِلَّا كَانُوا بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿29﴾ أَلَمْ يَرَوْا كَمْ أَهْلَكْنَا قَبْلَهُم
مِّنَ الْقُرُونِ أَنَّهُمْ إِلَيْهِمْ لَا يَرْجِعُونَ ﴿30﴾ وَإِن كُلٌّ لَّمَّا جَمِيعٌ
لَّدَيْنَا مُحْضَرُونَ ﴿31﴾ وَءَايَةٌ لَّهُمُ الْأَرْضُ الْمَيْتَةُ أَحْيَيْنَاهَا وَأَخْرَجْنَا
مِنْهَا حَبًّا فَمِنْهُ يَأْكُلُونَ ﴿32﴾ وَجَعَلْنَا فِيهَا جَنَّاتٍ مِّن نَّخِيلٍ
وَأَعْنَابٍ وَفَجَّرْنَا فِيهَا مِنَ الْعُيُونِ ﴿33﴾ لِيَأْكُلُوا مِن ثَمَرِهِۦ
وَمَا عَمِلَتْهُ أَيْدِيهِمْ أَفَلَا يَشْكُرُونَ ﴿34﴾ سُبْحَانَ الَّذِي
خَلَقَ الْأَزْوَاجَ كُلَّهَا مِمَّا تُنۢبِتُ الْأَرْضُ وَمِنْ أَنفُسِهِمْ
وَمِمَّا لَا يَعْلَمُونَ ﴿35﴾ وَءَايَةٌ لَّهُمُ اللَّيْلُ نَسْلَخُ مِنْهُ النَّهَارَ
فَإِذَا هُم مُّظْلِمُونَ ﴿36﴾ وَالشَّمْسُ تَجْرِي لِمُسْتَقَرٍّ لَّهَا
ذَٰلِكَ تَقْدِيرُ الْعَزِيزِ الْعَلِيمِ ﴿37﴾ وَالْقَمَرُ قَدَّرْنَاهُ مَنَازِلَ حَتَّىٰ
عَادَ كَالْعُرْجُونِ الْقَدِيمِ ﴿38﴾ لَا الشَّمْسُ يَنۢبَغِي لَهَا أَن تُدْرِكَ
الْقَمَرَ وَلَا اللَّيْلُ سَابِقُ النَّهَارِ وَكُلٌّ فِي فَلَكٍ يَسْبَحُونَ ﴿39﴾

27. Bamu saukar da wata runduna daga ama ta Mala'iku ba, a bisa mutanensa (Habibun Najjari bayan mutuwa tasa), bamu kasance masu saukar da Mala'iki (saboda halakar da wani ba).
28. Uƙubarsu bata kasance ba illa tsawa guda ɗaya (ta Jibrilu), sai gasu suna mace.

(SHASHIN MABAIYANAR IKON ALLAH)

29. Yace "Ya nadama bisa bayi (waɗannan da makamaritansu, daga waɗanda suka ƙaryata mazanni aka halaka su, kiran nadama anan, ma'anarta, tsananin takaici), wanı manzo bazaizo musu ba face sun kasance suna izgili dashi, (wato wannan izgili dashi, (wato wannan izgili Shine sababin takaici wanda ya kai ga halakar dasu, wandashi kuma shiya sabauta musu tsananin takaici).
30. To (Shin mutanen Makka masu cewa "Lasta mursalan") basu ga daya wa muka halakar daga tsareku (wato al'ummatai) gaba-ninsu ba? kuma cewa haƙiƙa (su ababan halakarwan nan), bazasu koma izuwa ababan ƙaryatarwa ba?
31. Babu ɗaya daga talikai face dukkansu ababan hallarowa ne gare ni (cikin aron alƙiyama bayan tashin su daga ƙabari saboc sakamako).
32. Akwai aya a garesu cewa ƙasa;matacciya da muka raya ta (da ruwa) muka fitar da ƙwaya (kamar alkama) daga gareshi suke ci (wato shi ƙwayar.Wato a cikin wannan akwai aya a kan tashin alƙiyama).
33. Mun sanya gonakai a cikinta na daga dabinai da inabai a cikinta, mun ɓuɓɓugar da idanuwa cikinta (wato daga shashinta).
34. Donsu ci daga dabinan da ina ban nan, ba hannun su ce ta halicci waɗannan itatuwa ba, Shin basa godewa (ni'imomin Ubamgiji a garesu) ba?
35. Tsarki ya tabbatarwa Sarkin daya halicci dangogi dukkanta daga abinda ƙasa take tsagawa (na ƙwaya da waninta) kuma ya halitta daga kawukan su (na maza da mata), kuma ya halitta na daga abinda basu sani ba, (wato ababan halitta baƙi, kamar ƙage-ƙagen wannan zamani, motoci, talabijin da maka mantansu).
36. Ayacewa dare muna fito da rana daga gareshi (ayace babba a garesu, a bisa ƙudura mai girma), sai gasu sun shiga cikin duhu.
37. Rana tana gudana izuwa ƙarshenta, (daga cikin ikon Allah ta'ala, yana daga jimlar ayoyi a garesu Wata ma kamar haka, wato tana gudana izuwa matabbacinta wanda bazata ketare shi ba). Wancanenka gudu, gwaninta ne na Sarki Mabuwayi (a cikin mulkinsa) Masani (da halittarsa).
38. Wata mun kaddara shi masaukai (guda ishirin da takwas (28) a cikin dare ishirin da takwas (28) daga kowane wata, zai ɓuya dare biyu, in wato ya kasance kwana talatin, kuma zai ɓuya dare ɗaya in ya kasance kwana ashirin da tara), har yakoma a ganin idanu kamar zarba tsohuwa, (kamar zarbar dabino in ya tsufa, saboda in ya tsufa sai yayi siriri, yayi baka, yayi ƙanƙanta).
39. Rana bai kamata gareta ta riski wata (su tattara a guri ɗaya), dare bai ƙasance ya rigayi rana ba, (dare bazai zobasai bayan ƙarewar rana), kowanne (na daga rana da wato da taurari) suna cikin falaƙi (kewayayye) suna nunƙaya.

وَءَايَةٌ لَّهُمْ أَنَّا حَمَلْنَا ذُرِّيَّتَهُمْ فِي الْفُلْكِ الْمَشْحُونِ ﴿٤٠﴾ وَخَلَقْنَا
لَهُم مِّن مِّثْلِهِۦ مَا يَرْكَبُونَ ﴿٤١﴾ وَإِن نَّشَأْ نُغْرِقْهُمْ فَلَا صَرِيخَ لَهُمْ
وَلَا هُمْ يُنقَذُونَ ﴿٤٢﴾ إِلَّا رَحْمَةً مِّنَّا وَمَتَٰعًا إِلَىٰ حِينٍ ﴿٤٣﴾
* وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ اتَّقُوا مَا بَيْنَ أَيْدِيكُمْ وَمَا خَلْفَكُمْ
لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ ﴿٤٤﴾ وَمَا تَأْتِيهِم مِّنْ ءَايَةٍ مِّنْ ءَايَٰتِ
رَبِّهِمْ إِلَّا كَانُوا عَنْهَا مُعْرِضِينَ ﴿٤٥﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ أَنفِقُوا مِمَّا رَزَقَكُمُ
اللَّهُ قَالَ الَّذِينَ كَفَرُوا لِلَّذِينَ ءَامَنُوا أَنُطْعِمُ مَن لَّوْ يَشَآءُ
اللَّهُ أَطْعَمَهُۥ إِنْ أَنتُمْ إِلَّا فِي ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٤٦﴾ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ
هَٰذَا الْوَعْدُ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٤٧﴾ مَا يَنظُرُونَ إِلَّا صَيْحَةً وَاحِدَةً
تَأْخُذُهُمْ وَهُمْ يَخِصِّمُونَ ﴿٤٨﴾ فَلَا يَسْتَطِيعُونَ تَوْصِيَةً وَلَا إِلَىٰ
أَهْلِهِمْ يَرْجِعُونَ ﴿٤٩﴾ وَنُفِخَ فِي الصُّورِ فَإِذَا هُم مِّنَ الْأَجْدَاثِ
إِلَىٰ رَبِّهِمْ يَنسِلُونَ ﴿٥٠﴾ قَالُوا يَٰوَيْلَنَا مَنۢ بَعَثَنَا مِن مَّرْقَدِنَا هَٰذَا مَا وَعَدَ
الرَّحْمَٰنُ وَصَدَقَ الْمُرْسَلُونَ ﴿٥١﴾ إِن كَانَتْ إِلَّا صَيْحَةً وَاحِدَةً
فَإِذَا هُمْ جَمِيعٌ لَّدَيْنَا مُحْضَرُونَ ﴿٥٢﴾ فَالْيَوْمَ لَا تُظْلَمُ نَفْسٌ
شَيْـًٔا وَلَا تُجْزَوْنَ إِلَّا مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٥٣﴾

ثمن

40. Haƙiƙa cewa mu mun cika jirgin (Annabi Nuhu) halittu ayace garesu (mai nuna girman ƙudurar mu).
41. Munhalitta daga irinsa, (wato misalin jirgin Annabi Nuhu), Shine abinda suka aikatashi a bisa kamanninsa na jiraga ƙanana da manya), wato abinda suke hawa (a cikinsa).
42. In mun ga dama zamu nutsar dasu, (tareda samar da jiragan), to ba mai taimako a garesu su baza a tsamo su (daga azaba ba).
43. Sai don jinƙai daga garemu da hutawa da jin daɗi izuwa wani lokaci (wato izuwa ƙarewar ajalin su).

(AMBATON BA'ALIN HALULUWAN KAFIRAI)

44. In Ance dasu, "kuji tsoron abinda yake gabanku (na daga azabar duniya, kamar waninsu), da abinda yake bayanku (na daga azabar lahira), don ku sami jinƙan Ubangiji" (saisu bijire ga buran gasgatawa).
45. Babu wata aya daga ayoyin Ubangijinsu datazo musu, face sun kasance masu bijirewa ga buranta.
46. Idan Fuƙara'us-sahabati sukace dasu "Ku ciyar daga abinda Allah ya azurta muku (a garemu na daga dukiyoyi) waɗanda suka kafirta, zasu faɗa ga waɗanda suka bada gaskiya (don izgili a garesu), Shin. yanzu ma ciyar da wanda da Allah yaga dama da saiyaci dashi, (a cikin ƙudurin ku wannan?) kai ku dai baku kasance a cikin Bata mabayyani.
47. Suna cewa "Yaushe ne wannan alkawari (na tashin Alƙiyama), inkun kasance masu gaskiya (a cikinsa).
48. Ubangiji yace, "Basa sauraren komai illa busa guda ɗaya (ta israfila, Itace busar Israfila ta far-ko), ta danke su alhali su, suna husuma da juna.
49. Bazasu sami damar yin wasiyya ba, bazasu iyakomawa (izuwa gidan su badaga kasu-woyinsu da shagulgulansu, bari su mutuwa zasuyia cikinta).
50. Zayi busa (Shine busa ta biyu saboda tashin alƙiyama shekara arba'in ne tsakanin busar guda biyu), sai gasu (ababan yiwa gargaɗin nan) daga cikin ƙaburbura, suna fitowa.
51. Kafirai daga cikinsu sukace "Ya halakarmu! Waya tashe mu daga gurin kwanciyarmu, (daga ƙaburburan mu? Don sun ,a cikin ƙaburburan suna masu barci ba a farayi muzu azabasai sun farka), wannan tashi Shine Ubangiji yayi alkawari dashi, ma'aikan Allah sun gasgata (a cikinsa, sun yi furici bazai amfane su ba).
52. (Ana cewa dasu), "bata kasance ba illa tsawa guda ɗaya" (wato busa, wannan maganar Israfilu ce) sai gasu gaba ɗayansu ababan kawo wa ne nan garemu, (wato Israfilu zaice "Yake waɗannan ƙasusuwa rididdigag-giya da jijiyoyi wacce ta yanyanke da ƙasusuwa waɗanda suke daban-daban da gasu waɗanda suka kekkece, haƙiƙa Ubangiji yana umarninku ku tattara rabe hukunci).
53. A yau baza a sakawa kai basai sakamakon abinda suka kasance suna aikatawa.

ربع

إِنَّ أَصْحَٰبَ ٱلْجَنَّةِ ٱلْيَوْمَ فِي شُغُلٍ فَٰكِهُونَ ﴿54﴾ هُمْ
وَأَزْوَٰجُهُمْ فِي ظِلَٰلٍ عَلَى ٱلْأَرَآئِكِ مُتَّكِـُٔونَ ﴿55﴾ لَهُمْ
فِيهَا فَٰكِهَةٌ وَلَهُم مَّا يَدَّعُونَ ﴿56﴾ سَلَٰمٌ قَوْلًا مِّن رَّبٍّ
رَّحِيمٍ ﴿57﴾ وَامْتَٰزُواْ ٱلْيَوْمَ أَيُّهَا ٱلْمُجْرِمُونَ ﴿58﴾ * أَلَمْ أَعْهَدْ
إِلَيْكُمْ يَٰبَنِيٓ ءَادَمَ أَن لَّا تَعْبُدُواْ ٱلشَّيْطَٰنَ إِنَّهُۥ لَكُمْ عَدُوٌّ
مُّبِينٌ ﴿59﴾ وَأَنُ اعْبُدُونِي هَٰذَا صِرَٰطٌ مُّسْتَقِيمٌ ﴿60﴾ وَلَقَدْ
أَضَلَّ مِنكُمْ جِبِلًّا كَثِيرًا أَفَلَمْ تَكُونُواْ تَعْقِلُونَ ﴿61﴾ هَٰذِهِۦ
جَهَنَّمُ ٱلَّتِي كُنتُمْ تُوعَدُونَ ﴿62﴾ ٱصْلَوْهَا ٱلْيَوْمَ بِمَا كُنتُمْ
تَكْفُرُونَ ﴿63﴾ ٱلْيَوْمَ نَخْتِمُ عَلَىٰٓ أَفْوَٰهِهِمْ وَتُكَلِّمُنَآ أَيْدِيهِمْ
وَتَشْهَدُ أَرْجُلُهُم بِمَا كَانُواْ يَكْسِبُونَ ﴿64﴾ وَلَوْ نَشَآءُ لَطَمَسْنَا
عَلَىٰٓ أَعْيُنِهِمْ فَاسْتَبَقُواْ ٱلصِّرَٰطَ فَأَنَّىٰ يُبْصِرُونَ ﴿65﴾ وَلَوْ نَشَآءُ
لَمَسَخْنَٰهُمْ عَلَىٰ مَكَانَٰتِهِمْ فَمَا ٱسْتَطَٰعُواْ مُضِيًّا وَلَا يَرْجِعُونَ ﴿66﴾
وَمَن نُّعَمِّرْهُ نَنكُسْهُ فِي ٱلْخَلْقِ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿67﴾ وَمَا
عَلَّمْنَٰهُ ٱلشِّعْرَ وَمَا يَنۢبَغِي لَهُۥٓ إِنْ هُوَ إِلَّا ذِكْرٌ وَقُرْءَانٌ مُّبِينٌ ﴿68﴾
لِّتُنذِرَ مَن كَانَ حَيًّا وَيَحِقَّ ٱلْقَوْلُ عَلَى ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿69﴾

('YAN WUTADA 'YAN ALJANNA)

54. Haƙiƙa 'yan Aljanna suna cikin shagali (ga buran abinda 'yan wuta suke ciki suna cikin shagulgula na jin daɗi kamar farke 'yammata ba shagali na wahala ba domin aljanna ba wahala cikinta, mani'imta.
55. Su da matayensu suna cikin inuwiyi, (rana bata taɓa su), suna kan gadaje suna masu dogaro a kan matasan kai.
56. Abib marmari na garesu a cikinta, duk abinda suke buri na garesu (a cikina).
57. Sai suji magana daga Ubangiji mai jinƙai yana ce dasu "Salamun alaikum".
58. (Yana cewa dasu) "Ku ware guri ɗaya, yaku ma'abuta laifi, ku kaɗaita daga muminai yayin da suka cuɗanya dasu).
59. Shin ban umarce ku bane yaku bani Adama! na ce, "kadaku ,bautawa Shaiɗan? Haƙiƙa magauci ne gareku mabayyanin ƙiyayya".
60. "Kuma ku bauta mini (kubini, wato ku ɗayanta ni, kuyi biyayya ga reni) wannan ta farki ne madaidaici".
61. Haƙiƙa ya ɓatar da halitta mai yawa daga garcku, Shinbaku kasance kuna "hankaltar ɓatarwar sa ba?)".
62. Wannan Jahannama ce wacce aka kasance anayi muku alkawari da ita. (A lahira za a gaga musu haka).
63. "Ku shigeta a yau saboda kasance-warku kafirai".
64. A yau ne muke yimƙewa bakunansu (su kafirai saboda faɗin su Wallahi Allah bamu kasance masu shirka ba), hannayensu zasuyimana zance, ƙafafuwansu zasuyimana magana da waninta zasuyishaida da abinda suka gabata (kowace gaɓa zata bayyanar da abindata gabatar).

(FALALAR UBANGIJI BISA MUTANE MAIGIRMA CE)

65. Da mun ga dama, da munyi dumɗiya a kan idanuwansa, (wato mun shafe idonsu su zama sumul, makafi, masu shafaffen ido), su gaggauci hanya (izuwa gidako unguwa kamar da suka saba), Yaya zasu ga gabansu a yayin nan? (Bazasu ganiba).
66. Da mun ga dama da mun canja halittarsu (su zama birrai ko alhanzirai, ko duwarwatsu) a bisa yadda suke a gidaddajinsu, bazasu sami damar kai-kawo ba, bazasu sami damar komawa (izuwa gida ba, in sun fita).
67. Wanda muka tsawaita ransa ma tauye shi (wato ma sunkuyar dashi) a cikin halitta (ya zama rarrauna tsoho, bayan ƙarfi da ƙuruciya). Shin basayi hankali ba, mai ikone bisa tashin alƙiyama).

(TABBATAR DA WAHADINIYAGA ALLAH DA KORE WAƘA)

68. Bamu sanar da Annabi Sallallahu alaihi wa sallama ta watca ba, (raddi ne ga maganar su cewa abinda Annabi Sallallahu alaihi wa sallama yazo dashi waƙa ne), to, waƙa baza tayiwu a gareshi ba, shi bai kasance basai gargaɗi da Kur'ani mabayyanin hukuncc-hukence.
69. Don yagargadar da wanda ya kasance mai rai dashi (sune muminai), azabata tabbata ga kafirai (Waɗandasu kamar matattune, basa hankaltar (abinda ake musu gargaɗi dashi).

أَوَلَمْ يَرَوْا أَنَّا خَلَقْنَا لَهُم مِّمَّا عَمِلَتْ أَيْدِينَا أَنْعَامًا
فَهُمْ لَهَا مَالِكُونَ ﴿٧١﴾ وَذَلَّلْنَاهَا لَهُمْ فَمِنْهَا رَكُوبُهُمْ
وَمِنْهَا يَأْكُلُونَ ﴿٧٢﴾ وَلَهُمْ فِيهَا مَنَافِعُ وَمَشَارِبُ
أَفَلَا يَشْكُرُونَ ﴿٧٣﴾ وَاتَّخَذُوا مِن دُونِ اللَّهِ آلِهَةً لَّعَلَّهُمْ يُنصَرُونَ ﴿٧٤﴾
لَا يَسْتَطِيعُونَ نَصْرَهُمْ وَهُمْ لَهُمْ جُندٌ مُّحْضَرُونَ ﴿٧٥﴾
فَلَا يَحْزُنكَ قَوْلُهُمْ إِنَّا نَعْلَمُ مَا يُسِرُّونَ وَمَا يُعْلِنُونَ ﴿٧٦﴾
* أَوَلَمْ يَرَ الْإِنسَانُ أَنَّا خَلَقْنَاهُ مِن نُّطْفَةٍ ثمن
فَإِذَا هُوَ خَصِيمٌ مُّبِينٌ ﴿٧٧﴾ وَضَرَبَ لَنَا مَثَلًا وَنَسِيَ خَلْقَهُ
قَالَ مَن يُحْيِي الْعِظَامَ وَهِيَ رَمِيمٌ ﴿٧٨﴾ قُلْ يُحْيِيهَا
الَّذِي أَنشَأَهَا أَوَّلَ مَرَّةٍ وَهُوَ بِكُلِّ خَلْقٍ عَلِيمٌ ﴿٧٩﴾
الَّذِي جَعَلَ لَكُم مِّنَ الشَّجَرِ الْأَخْضَرِ نَارًا
فَإِذَا أَنتُم مِّنْهُ تُوقِدُونَ ﴿٨٠﴾ أَوَلَيْسَ الَّذِي خَلَقَ السَّمَاوَاتِ
وَالْأَرْضَ بِقَادِرٍ عَلَىٰ أَن يَخْلُقَ مِثْلَهُم بَلَىٰ وَهُوَ الْخَلَّاقُ الْعَلِيمُ ﴿٨١﴾
إِنَّمَا أَمْرُهُ إِذَا أَرَادَ شَيْئًا أَن يَقُولَ لَهُ كُن فَيَكُونُ ﴿٨٢﴾
فَسُبْحَانَ الَّذِي بِيَدِهِ مَلَكُوتُ كُلِّ شَيْءٍ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٨٣﴾

70. Shin basu sani ba cewa haƙiƙa mu, mun halicci dabbobi (wato raƙuma da shanu da tumakai donsu, daga abinda hannayen mu (wato ikon mu) ta aikata,(bada abokin tarayyako mataimaki ba), to su mana llaka ne gareta.

71. Mun hore ta garesu, abin haw-ansu yana daga cikinta, suna ci daga gareta.

72 . Suna da amfanuwa, (wato am-fanunuwa) na garesu a cikinta, (kamar gasusuwanta). Shin bazasu godewa (mai ni'imta su da ita su bada gaskiya ba?).

73. Sun riƙi iyayen giji ba Allah ba (gumaka dasuke bauta mata, domin su tsaresu daga azabar Allah) don a hana musu azabar Allah.

74. Basu da ikon taimakon iyayen gijin nan nasu, su, iyayen gijin nan na daga gumaka runduna ce ta-su, ababan kai wa ne cikin wuta tare dasu.

75. Kada faɗin su (cewa Lasta mursalan da waninsa) ya baƙanta maka rai, haƙiƙa mu mun san abinda suke bayyanawa da abinda suke ɓoyewa.

(TABBATAR DA TASHIN ALƘIYAMA)

76. Shin mutum (wato Asi dan Wa'ilu) bai sani bane? Haƙiƙa mu mun halicce shi daga nudiifa, (ɗigon kazanta, har muka maidashi ƙaƙƙarfa), sai gashi mai tsananin husuma (a cikin alƙiyama?).

77. Yasanya misali garemu (a cikin wancanenka), ya mance halitta tasa (daga maniyi wandashi yafi baƙunci daga mayar da ƙamarsa), yace, "Wa yake raya kasusuwa alhali ita tana riduddi-gaggiya?" (An ruwaito cewa shiya riƙi wani ƙashi riduddugaggc ya mitstsikc shi yace da Annabi (Sallallahu alaihi wa sallama) "Kana ganin Allah ya raya wan-nan bayan ya ridudduge?" Manzon Allah yace, "Na'am, kuma ya shigar dakai wuta").

78. Cene, "Wanda ya fareta marrar farko Shine mai rayata. Shi masanine da komai (a rarrabc da a dunƙule tun gaban halittarsa da bayan halittarsa").

79. Wanda yasanya muku wuta a cikin jimlar mutane daga itaciya (Shine yaɗiya), kuma daga dukkan itaciya sai namanama) sai ga ku kuna hura wuta daga shi, (wannan mai shiryarwa ne bisa tashin alƙiyama saboda Ubangiji ya shirya tsakanin ruwa da wutada Itace, ruwa bai kashe wuta ba, wuta bata ƙone Itace ba).

80. Yanzu wanda ya halicci sammai da ƙassai (tareda girmansu)ba mai iko bane bisa ya halicci tankassu ba? (Wato mutane don ƙanƙanta) Mai ikonc bisa wancanenka, (ya amsawa kansa ga kansa). Ubangiji shi mai yanau halitta ne, masani (da komai).

81. Dahir al'amarinsa dai idan yanufi wani abu sai yacc da abin "zamo", saiya samu.

82. Tsarki ya tabbatarwa Sarkin da tsananin mallakar komai yake ikonsa, kuma izuwa gareshi za a koma (daku ,a ranar lahira).

37 سُورَةُ الصَّافَّاتِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ مِائَةٌ وَاحِدَىٰ وَثَمَانُونَ ءَايَةً 181

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

وَالصَّافَّاتِ صَفًّا ﴿1﴾ فَالزَّاجِرَاتِ زَجْرًا ﴿2﴾ فَالتَّالِيَاتِ ذِكْرًا ﴿3﴾ إِنَّ إِلَٰهَكُمْ
لَوَاحِدٌ ﴿4﴾ رَبُّ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا وَرَبُّ الْمَشَارِقِ ﴿5﴾
إِنَّا زَيَّنَّا السَّمَاءَ الدُّنْيَا بِزِينَةٍ الْكَوَاكِبِ ﴿6﴾ وَحِفْظًا مِّن كُلِّ شَيْطَانٍ مَّارِدٍ ﴿7﴾
لَّا يَسَّمَّعُونَ إِلَى الْمَلَإِ الْأَعْلَىٰ وَيُقْذَفُونَ مِن كُلِّ جَانِبٍ ﴿8﴾
دُحُورًا وَلَهُمْ عَذَابٌ وَاصِبٌ ﴿9﴾ إِلَّا مَنْ خَطِفَ الْخَطْفَةَ فَأَتْبَعَهُ شِهَابٌ ثَاقِبٌ ﴿10﴾
فَاسْتَفْتِهِمْ أَهُمْ أَشَدُّ خَلْقًا أَم مَّنْ خَلَقْنَا إِنَّا خَلَقْنَاهُم مِّن طِينٍ لَّازِبٍ ﴿11﴾
بَلْ عَجِبْتَ وَيَسْخَرُونَ ﴿12﴾ وَإِذَا ذُكِّرُوا لَا يَذْكُرُونَ ﴿13﴾ وَإِذَا رَأَوْا آيَةً يَسْتَسْخِرُونَ ﴿14﴾
وَقَالُوا إِنْ هَٰذَا إِلَّا سِحْرٌ مُّبِينٌ ﴿15﴾ أَءِذَا مِتْنَا وَكُنَّا تُرَابًا وَعِظَامًا
إِنَّا لَمَبْعُوثُونَ ﴿16﴾ أَوَءَابَاؤُنَا الْأَوَّلُونَ ﴿17﴾ قُلْ نَعَمْ وَأَنتُمْ دَاخِرُونَ ﴿18﴾
فَإِنَّمَا هِيَ زَجْرَةٌ وَاحِدَةٌ فَإِذَا هُمْ يَنظُرُونَ ﴿19﴾ وَقَالُوا يَا وَيْلَنَا هَٰذَا يَوْمُ الدِّينِ ﴿20﴾
هَٰذَا يَوْمُ الْفَصْلِ الَّذِي كُنتُم بِهِ تُكَذِّبُونَ ﴿21﴾ * احْشُرُوا الَّذِينَ ظَلَمُوا وَأَزْوَاجَهُمْ
وَمَا كَانُوا يَعْبُدُونَ ﴿22﴾ مِن دُونِ اللَّهِ فَاهْدُوهُمْ إِلَىٰ صِرَاطِ الْجَحِيمِ ﴿23﴾ وَقِفُوهُمْ إِنَّهُم مَّسْئُولُونَ ﴿24﴾

ربع

Wannan Suratul Yakdinu ce
A Makka aka. saukar da ita Aya Dari da Tamanin da Biyuce (182)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a lahira a keɓe

Ita wannan sura taƙunshi zance kan Tauhidi da Tashin Alƙiyama da Zance kan Mushurikai da Halulu-wansa a Duniya da Lahira da Zance kan Tabbatar Annabci da Zance kan Muminai da Haluluwansu a Duniya da Lahira da Ambaton Kissoshin ba'alin Annabawa da Al'umominsu da Karfafa ƙudirin aniyar Musulmi da Raunana ƙarfin Kafirai. (HAƘIƘA UBANGIJI DAYA NE, ALƘIYAMA GASKIYACE)

1. Ubangiji ya rantse da Mala'iku masu jera sahu a cikin ibida, jerawa.
2. Haka Mala'iku masuyin tsawa (ga girgije) tsawa.
3. Kuma haka masu karantawar (alƙur'ani Mala'iku ko waninsu) don gargaɗi.
4. Haƙiƙa Ubangijinku guda ɗaya ne.
5. Ubangijin sammai da ƙassaida abinda yake Tsakaninsu, Ubangijin mahudar rana da mafaɗarta. (Rana tana da mahudai da mafaɗai a kowane wuni).
6. Haƙiƙa mun ƙawata saman duniya da adon taurari.
7. Mun kiyayetada taurari kiyayewa daga kowane shaiɗani mai taurin kai.
8. Bazasuyisauraro izuwa Mala'ikun sama ba. Ana jefe su daga kowacce nahiya (da taurari na daga sassan sama).
9. Ababan korewa, suna da azaba madauwamiya a lahira.
10. Sai wanda ya fauta guda ɗaya daga Mala'iku, kuma tauraro mai tsananin haske yabi shi (y hudashi).
11. To tambaye su (wato kafirai Makka, shin) sune sukafi ƙarfin halitta, ko waɗanda muk halitta (na Mala'ikuda samme da ƙassaida abinda yake cikin su), haƙiƙa mun halicci asalii su Annabi Adamu daga taɓo ms danƙo. Su daina girman kai d musun alƙur'ani da Annabi sa boda halittar su rarrauna ce wannan musu kuma mai halaka dasune nan da nan).
12. Kai, dai kayi mana ki ne (Sal lallahu alaihi wa sallama) dag ƙaryata ka dasuke yi, su kum suna yin ba'a daga mana kin ka
13. Idan an gargaɗe su da alƙur'ani basa gargaɗuwa.
14. In sun ga aya (kamar tsagewa wata) suna izgili da ita.
15. Saisu ce a cikinta, "wannan bakasance basai tsafi mabayya ni", (saisu faɗa suna musun tashin alƙiyama).
16. "Idan mun mutu, mun zama turɓaya da kasusuwa, shin haƙiƙa mu lallai za a tashe mu?" 17. "Ko iyayenmune farko?".
18. Cene, "na'am za a tashe ku alhali kuna wulaƙantattu".
19. Ai ita dai kalma ce guda ɗaya kawai sai ga talikai rayayyu suna duban (abindaza ayi dasu).
20. Sai kafirai su ce, "Ya halakar mu" (sai Mala'iku su ce dasu) "Wannan Shine ranar sakamako".
21. "Wannan Shine ranar rabe hukunci wanda huka kasance kuna ƙaryatawa dashi". (WANI ABU DAGA MATSAYIN MUSHURIKAI RANAR ALƘIYAMA)
22. (Ana cewa da Mala'iku) "Ku tattara Shaiɗanu da abinda suka kasance suna bautawa na dag gumaka.
23. "Ba Allah ba, ku shiryar da zi izuwa tafarkin wutar Jahanna ma".
24. "Ku tsaresu (nan ga siraɗi) Haƙiƙa su ababan tambayo ne (ga dukkan maganganunsu ds ayyukansu, ana faɗa musu dor umstawa wato zargi).

مَا لَكُمْ لَا تَنَاصَرُونَ ﴿25﴾ بَلْ هُمُ الْيَوْمَ مُسْتَسْلِمُونَ ﴿26﴾ وَأَقْبَلَ بَعْضُهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ
يَتَسَآءَلُونَ ﴿27﴾ قَالُوا إِنَّكُمْ كُنتُمْ تَأْتُونَنَا عَنِ الْيَمِينِ ﴿28﴾ قَالُوا بَل لَّمْ تَكُونُوا مُؤْمِنِينَ ﴿29﴾
وَمَا كَانَ لَنَا عَلَيْكُم مِّن سُلْطَانٍ بَلْ كُنتُمْ قَوْمًا طَاغِينَ ﴿30﴾ فَحَقَّ
عَلَيْنَا قَوْلُ رَبِّنَا إِنَّا لَذَآئِقُونَ ﴿31﴾ فَأَغْوَيْنَاكُمْ إِنَّا كُنَّا غَاوِينَ ﴿32﴾
فَإِنَّهُمْ يَوْمَئِذٍ فِي الْعَذَابِ مُشْتَرِكُونَ ﴿33﴾ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَفْعَلُ بِالْمُجْرِمِينَ ﴿34﴾
إِنَّهُمْ كَانُوا إِذَا قِيلَ لَهُمْ لَا إِلَٰهَ إِلَّا اللَّهُ يَسْتَكْبِرُونَ ﴿35﴾ وَيَقُولُونَ
أَئِنَّا لَتَارِكُوا آلِهَتِنَا لِشَاعِرٍ مَّجْنُونٍ ﴿36﴾ بَلْ جَآءَ بِالْحَقِّ وَصَدَّقَ الْمُرْسَلِينَ ﴿37﴾
إِنَّكُمْ لَذَآئِقُوا الْعَذَابِ الْأَلِيمِ ﴿38﴾ وَمَا تُجْزَوْنَ إِلَّا مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿39﴾
إِلَّا عِبَادَ اللَّهِ الْمُخْلَصِينَ ﴿40﴾ أُولَٰئِكَ لَهُمْ رِزْقٌ مَّعْلُومٌ ﴿41﴾ فَوَاكِهُ
وَهُم مُّكْرَمُونَ ﴿42﴾ فِي جَنَّاتِ النَّعِيمِ ﴿43﴾ عَلَىٰ سُرُرٍ مُّتَقَابِلِينَ ﴿44﴾
يُطَافُ عَلَيْهِم بِكَأْسٍ مِّن مَّعِينٍ ﴿45﴾ بَيْضَآءَ لَذَّةٍ لِّلشَّارِبِينَ ﴿46﴾ لَا فِيهَا
غَوْلٌ وَلَا هُمْ عَنْهَا يُنزَفُونَ ﴿47﴾ وَعِندَهُمْ قَاصِرَاتُ الطَّرْفِ عِينٌ ﴿48﴾
كَأَنَّهُنَّ بَيْضٌ مَّكْنُونٌ ﴿49﴾ فَأَقْبَلَ بَعْضُهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ يَتَسَآءَلُونَ ﴿50﴾
* قَالَ قَآئِلٌ مِّنْهُمْ إِنِّي كَانَ لِي قَرِينٌ ﴿51﴾ يَقُولُ أَئِنَّكَ لَمِنَ الْمُصَدِّقِينَ ﴿52﴾ أَئِذَا مِتْنَا ثمن
وَكُنَّا تُرَابًا وَعِظَامًا أَئِنَّا لَمَدِينُونَ ﴿53﴾ قَالَ هَلْ أَنتُم مُّطَّلِعُونَ ﴿54﴾ فَاطَّلَعَ فَرَءَاهُ فِي سَوَآءِ الْجَحِيمِ ﴿55﴾

25. "Me ke gareku ba kwa taimakon juna (tamfar da kuke a duniya? Ana cewa dasu har yau). 26. "Bari su yau masu jawuwa ne a wulaƙance".27. Shashinsu yagabato da sashi suna tambayeyeniya (wato zargin juna da husuma). 28. Su mabiya daga cikinsu suka faɗa ga waɗanda suke bi, " haƙiƙa ku kun kasance kunazo mana bisa jihar ƙarfi (wato kune kuka ɓashshe mu)". 29. Sai ababan bin sukace (dasu) "Kai ku ɗai baku kasance munimai ba (don ba a ɓad da wanda ba muminine ba)".
30. "Ba wata hujja data kasance garemu a kanku wadda zamu tilashe ku a kan bin mu, Bari ku kun kasance mutane masu shishshigi".31. "Maganar Ubangijin mu ta tabbata kan mu baki ɗaya, (Shine faɗin sa lallai zan cika Jahannama da mutane da aljanu baki daya) haƙiƙa mu baki ɗaya zamu danɗani (azabasaboda wannan magana kuma don haka ne sukace)". 32. "Sai muka ɓatar daku ,don saboda haƙiƙa mu, mun kasance batattu".33. Sai Ubangiji yace, "To, haƙiƙa su a wannan rana masu tattara ne a cikin azaba".34. Haƙiƙa mu kamar yadda muka aikata ga waɗannan haka muke aikatawa ga masu laifi (waɗannan, wato muke wa mai daga cikinsu da waɗanda akabi muke yi musu azaba). 35. Haƙiƙa a su waɗannan sun ka sance in an ce, "LA ILAHA IL LALLAHU suna girman kai.
36. Suna cewa, "yanzu mu, haƙiƙa;lallai masu barin iyayen gijinmi ne don mawaƙi marar hankali (suna nufin Annabi Sallallahi alaihi wa sallama). 37. (Ubangiji ta'ala yace), "Yazo musu da gaskiya ne, yagasgata manzonni (waɗanda sukazo dashi, Shine LA ILAHA ILLALLA HU MUHAMMADU RASULUL LAHI".
38. Haƙiƙa ku lallai masu ɗanɗana azaba mai raɗaɗi (a ranar lahira ne.

(MASU IKHLASI SUNA ALJANNA)

39. Ba a sakamako sai sakamakor abinda suka ƙasance suna aika tawa. 40. Sai bayin Allah ababan tsarka kewa (masu tsarkakewan aik don Allah). 41. Wadancanenka arziki abin sani ya tabbata garesu (a cikin Aljanna safiya dayammaci).
42. Kayan marmari (Shine abinda ake cin don jin marmari ba don kiyaye lafiya ba, saboda 'yan aljanna mawadata ne ga kiyaye lafiya. Saboda Allah ya halicci jikkunansu don ababan) su ababan girmama wa ne (da sakamakon Ubangiji subhanahu wa Ta'ala). 43. Suna cikin aljannar ni'ima. 44. A kan gadaje suna masu duban juna. 45. Ana kewayo a garesu da gidauniya ta ruwan marmaro (na giyar aljanna da yake gudana a kan fuskar ƙasar aljanna, kamar ƙoramun ruwa).
46. Mai tsananin fari (ita wannan gi-dauniyar tafi nono fari), mai daɗi ga mashaya, (saɓanin giyar duniya, don ita mummuna ce yayin sha). 47. Ba motsa hankali a cikinta, sa bazasuyimaye ba, daga shanta, (saɓanin giyar duniya). 48. "Yanmata masu tsare idanuwansu suna garesu (basa duba izuwa wanin mazajen su, saboda kyan mazajen a gurin matan wato kowacce bata sha'awai wani namiji sai mijinta, wato za a fahimta daga wannan cewa zaman aljanna zama ne na iffa, wato kamun kai, baza tayiwu wasanni ya afku a cikinta daga maza ko mata ba) masu gadagadan idanu tareda kyanta. 49. Kai kace launin su 'yammats nan ƙwan jimina ne abin lulluɓewa (da gyawaska, ƙura bata saduwa izuwa gareshi. Launir wannan kwai wato fari a cikir 'yar anantaka, Shine mafi kyar launonin mata). 50. Sai shashin 'yan aljanna yagabato bisa shashi suna tambayai juna (ga abinda ya wuce dasu a cikin duniya, wato sun haɗu suna hira). 51. Mai magana daga cikinsu yace " Haƙiƙa ni wani aboki ya kasance gareni, (wato aboki wanda yake musun tashin alƙiyama). 52. "Yana cewa dani (don umzta ni), shin haƙiƙa ina cikin masu gasgatawa da tashin alƙiyama?". 53. "Yanzu idan mun mutu mun zama turɓaya da kasusuwa haƙiƙa mu ababan sakawa ne?".

قَالَ تَاللَّهِ إِن كِدتَّ لَتُرْدِينِ ﴿56﴾ وَلَوْلَا نِعْمَةُ رَبِّي لَكُنتُ مِنَ الْمُحْضَرِينَ ﴿57﴾
أَفَمَا نَحْنُ بِمَيِّتِينَ ﴿58﴾ إِلَّا مَوْتَتَنَا الْأُولَىٰ وَمَا نَحْنُ بِمُعَذَّبِينَ ﴿59﴾
إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ الْفَوْزُ الْعَظِيمُ ﴿60﴾ لِمِثْلِ هَٰذَا فَلْيَعْمَلِ الْعَامِلُونَ ﴿61﴾
أَذَٰلِكَ خَيْرٌ نُّزُلًا أَمْ شَجَرَةُ الزَّقُّومِ ﴿62﴾ إِنَّا جَعَلْنَاهَا فِتْنَةً لِّلظَّالِمِينَ ﴿63﴾
إِنَّهَا شَجَرَةٌ تَخْرُجُ فِي أَصْلِ الْجَحِيمِ ﴿64﴾ طَلْعُهَا كَأَنَّهُ رُءُوسُ الشَّيَاطِينِ ﴿65﴾
فَإِنَّهُمْ لَآكِلُونَ مِنْهَا فَمَالِئُونَ مِنْهَا الْبُطُونَ ﴿66﴾ ثُمَّ إِنَّ لَهُمْ عَلَيْهَا
لَشَوْبًا مِّنْ حَمِيمٍ ﴿67﴾ ثُمَّ إِنَّ مَرْجِعَهُمْ لَإِلَى الْجَحِيمِ ﴿68﴾ إِنَّهُمْ أَلْفَوْا آبَاءَهُمْ
ضَالِّينَ ﴿69﴾ فَهُمْ عَلَىٰ آثَارِهِمْ يُهْرَعُونَ ﴿70﴾ وَلَقَدْ ضَلَّ قَبْلَهُمْ أَكْثَرُ
الْأَوَّلِينَ ﴿71﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا فِيهِم مُّنذِرِينَ ﴿72﴾ فَانظُرْ كَيْفَ كَانَ عَاقِبَةُ
الْمُنذَرِينَ ﴿73﴾ إِلَّا عِبَادَ اللَّهِ الْمُخْلَصِينَ ﴿74﴾ وَلَقَدْ نَادَانَا نُوحٌ فَلَنِعْمَ الْمُجِيبُونَ ﴿75﴾
وَنَجَّيْنَاهُ وَأَهْلَهُ مِنَ الْكَرْبِ الْعَظِيمِ ﴿76﴾ وَجَعَلْنَا ذُرِّيَّتَهُ هُمُ الْبَاقِينَ ﴿77﴾
وَتَرَكْنَا عَلَيْهِ فِي الْآخِرِينَ ﴿78﴾ سَلَامٌ عَلَىٰ نُوحٍ فِي الْعَالَمِينَ ﴿79﴾ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجْزِي
الْمُحْسِنِينَ ﴿80﴾ إِنَّهُ مِنْ عِبَادِنَا الْمُؤْمِنِينَ ﴿81﴾ ثُمَّ أَغْرَقْنَا الْآخَرِينَ ﴿82﴾
* وَإِنَّ مِن شِيعَتِهِ لَإِبْرَاهِيمَ ﴿83﴾ إِذْ جَاءَ رَبَّهُ بِقَلْبٍ سَلِيمٍ ﴿84﴾ ربع
إِذْ قَالَ لِأَبِيهِ وَقَوْمِهِ مَاذَا تَعْبُدُونَ ﴿85﴾ أَئِفْكًا آلِهَةً دُونَ اللَّهِ تُرِيدُونَ ﴿86﴾

54. Sai wannan mai faɗa ya faɗa (ga ɗan'uwansa, yace), "Shin ku masu tsinkaye ne (taredani izu-wa wuta?" Sukace "A'a").55. Sai shiya duba (daga cikin tagogin 'yan aljanna) sai yaga abokin nasa a tsatstsakin jahannama. 56. sai yace dashi, (don ganganko gareshi yace dashi) "Wallahi ka kusa ka halakar dani. 57. "Ba don ni'imar Ubangijina (ga-reni daya ui mini da imani ba), dana kasance cikin ababan halartarwa (taredakai cikin wuta). 58. ('Yan aljanna saisu ce) "Shin to mu ba matattu bane"?.59. "Sai mutuwar mu ta fark (wacce ta kasance a duniya), kuma mu baza ayi mana azaba ba? (Tambayace da take bayyana ni'imar Allah a kan ba ayi musu azaba ba har abada). 60. Haƙiƙa wanna (abinda aka ambata ga 'yan aljanna) Lallai Shine rabo mai girma.
61. Saboda irin wannan, to masu aiki suyiaiki.

(JAHANNAMA CE MAKOMAR AZZALUMAI)

62. Shin wancanenka abin ambato garesu Shine yafi wajen garar baƙi, ko kuwa itaciyar zaƙumi? (Wato furan juji wacce aka ta-nada ga 'yan wuta?). 63. Haƙiƙa mu mun sanya ta fitina ga kafirai (mutane Makka, saboda sun ce wuta tana ƙone Itace yayakuma zata tsirar dashi? Basu san cewa mai iko ba abinda yake gaji dashi). 64. Haƙiƙa ita itaciyace da take fitowa cikin zurfin jahannama (rassanta,sun ɗaukaka izuwa can ƙasa). 65. Hudar ta (mai kamar hudar dabino), kai kace shi kawukan chaiɗanu ne (wato micizai, mai mnrnmunar magana).
66. Haƙiƙa su waɗannan kafirai masu ci ne da ita (tareda mininta, saboda tsananin yunwar su), to masu cika cukkuna ne daga gareta. 67. Sannan haƙiƙa lallai cuɗanye na ruwan zafi ya tabbata a garesu a kanta. 68. Sannan haƙiƙa makomar su lallai izuwa jahannama ne (anfahinci cewa su suna fitowa daga gareta saboda su sha wannan ruwa. kuma cewa ruwan a waje yake. ba a cikin jahannama ba),
69. Saboda su haƙiƙa sun sami iyayensu ɓatattu. 70. To su ana kora su a kan gurabansu. 71. Haƙiƙa mafi yawan mutanen farko sun bata gabansu
72. Haƙiƙa mun aiko masu gargaɗi a cikinsu. 73. Ka dubaka gani ƙaƙa ƙarshen ababan tsoratarwa ya kasance?. 74. Sai bayin Allah ababan tsarkakewa.

(ƘISSAR ANNABI NUHU ALAIHISSALAMU)

75. Haƙiƙa Annabi Nuhu ya kira mu (da faɗinsa ni abin rinjaye ne ka taimake ni), Madalla masu amsawa mu. 76. Muka tserar dashi da iyalinsa daga bakin ciki mai girma, (wato nutsewa). 77. Muka sanya zurriyattasa sune kaɗai suka ragu, (mutane dukkansu daga zurriyarsa ne yana da 'ya'ya guda uku samu uban Larabawa da Farisa mutanen Iran da Rum wato su ake ce dasu a yanzu Taryan da Hamu uban baƙaƙen fatu, dayafisu uban Turkawa da Khazaru wato tatar dayajuju da Majuju da sauran 'yan uwansu). 78. Muka bar kyakkyawan abin ambato gareshi cikin mutanen karshe (na Annabawa da al'umma har izuwa ranar alƙiyama). 79. Gaisuwa (daga garemu) ta tabbata ga Annabi Nuhu a cikin talikai.
80. Mu kamar haka muke sakawa masu kyakkyawan aiki.
81. Haƙiƙa shi (Annabi Nuhu) yana daga bayinmu masu cikakken imani.
82. Sannan muka nutsar da ragowar kafiran mutanensa.

(ƘISSAR ANNABI IBRAHIMU ALAIHISSALAMU)

83. Haƙiƙa Annabi Ibrahimu yana daga cikin jama'ar Annabi Nuhu (wato yana daga cikin waɗanda sukabi shi a asalin addini ko da yake tsakaninsu da nisa, shekara 2640 Dubu biyu da ɗari shida da arba'in Tsaka-ninsu akwai Annabi Huda da Annabi salihu gaban Annabi Nuhu akwai uku Idrisu dashisu da Adamu).
84. Zamanin dayazowa Ubangijinsa da zuciya sumul bashirka.
85. Lokacin dayace da babansa, (ubana haƙiƙa ko ammi), "Me kuke bautawa?.
86. "Shin ƙaryar banza iyayen giji ba Allah bakuke nufi?"

فَمَا ظَنُّكُم بِرَبِّ الْعَالَمِينَ (87) فَنَظَرَ نَظْرَةً فِي النُّجُومِ (88) فَقَالَ إِنِّي سَقِيمٌ (89)
فَتَوَلَّوْا عَنْهُ مُدْبِرِينَ (90) فَرَاغَ إِلَىٰ آلِهَتِهِمْ فَقَالَ أَلَا تَأْكُلُونَ (91) مَا لَكُمْ
لَا تَنطِقُونَ (92) فَرَاغَ عَلَيْهِمْ ضَرْبًا بِالْيَمِينِ (93) فَأَقْبَلُوا إِلَيْهِ يَزِفُّونَ (94) قَالَ أَتَعْبُدُونَ
مَا تَنْحِتُونَ (95) وَاللَّهُ خَلَقَكُمْ وَمَا تَعْمَلُونَ (96) قَالُوا ابْنُوا لَهُ بُنْيَانًا فَأَلْقُوهُ فِي الْجَحِيمِ (97)
فَأَرَادُوا بِهِ كَيْدًا فَجَعَلْنَاهُمُ الْأَسْفَلِينَ (98) وَقَالَ إِنِّي ذَاهِبٌ إِلَىٰ رَبِّي سَيَهْدِينِ (99)
رَبِّ هَبْ لِي مِنَ الصَّالِحِينَ (100) فَبَشَّرْنَاهُ بِغُلَامٍ حَلِيمٍ (101) فَلَمَّا بَلَغَ
مَعَهُ السَّعْيَ قَالَ يَا بُنَيَّ إِنِّي أَرَىٰ فِي الْمَنَامِ أَنِّي أَذْبَحُكَ
فَانظُرْ مَاذَا تَرَىٰ قَالَ يَا أَبَتِ افْعَلْ مَا تُؤْمَرُ سَتَجِدُنِي إِن شَاءَ اللَّهُ مِنَ الصَّابِرِينَ (102)
فَلَمَّا أَسْلَمَا وَتَلَّهُ لِلْجَبِينِ (103) وَنَادَيْنَاهُ أَن يَا إِبْرَاهِيمُ (104) قَدْ صَدَّقْتَ
الرُّؤْيَا إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجْزِي الْمُحْسِنِينَ (105) إِنَّ هَٰذَا
لَهُوَ الْبَلَاءُ الْمُبِينُ (106) وَفَدَيْنَاهُ بِذِبْحٍ عَظِيمٍ (107) وَتَرَكْنَا
عَلَيْهِ فِي الْآخِرِينَ (108) سَلَامٌ عَلَىٰ إِبْرَاهِيمَ (109) كَذَٰلِكَ نَجْزِي الْمُحْسِنِينَ (110)
إِنَّهُ مِنْ عِبَادِنَا الْمُؤْمِنِينَ (111) وَبَشَّرْنَاهُ بِإِسْحَاقَ نَبِيًّا مِّنَ الصَّالِحِينَ (112)
وَبَارَكْنَا عَلَيْهِ وَعَلَىٰ إِسْحَاقَ وَمِن ذُرِّيَّتِهِمَا مُحْسِنٌ وَظَالِمٌ لِّنَفْسِهِ مُبِينٌ (113)
* وَلَقَدْ مَنَنَّا عَلَىٰ مُوسَىٰ وَهَارُونَ (114) وَنَجَّيْنَاهُمَا وَقَوْمَهُمَا مِنَ الْكَرْبِ الْعَظِيمِ (115)

ثمن

87. "To meye zatonku Ubangijin talikai (zamanin da kuka bautawa waninsa? Kuna zaton ya barku ba uƙuba? A'a").**88.** (Su masana taurari ne suKafita izuwa wani idi nasu, suka bar abincinsu nan ga gumakan nasu sukace wai don tabarruki ne, in sun komo saisu ci. Sukace da Sayyidina Ibrahima fita tareda mu), sai yayi duba duba cikin taurari (donya wahimtar dasu cewa shiya dogara ne a kanta donsu dogara dashi).
89. Sai yace, "Ni da sannu zan yi rashin lafiya".**90.** Sai suka juyaga buransa izuwa idonsu suna gudu suna bada baya. **91.** Saiya tafi sumru izuwa iyayen gijinsu (Itacen gumaka, akwai abinci a gabanta, saiya faɗa don izgili) "Shin ba kwa ci bane?" (Basu ce dashi komai ba, yaji shiru). **92.** Sai yace, "Me ya same ku ba kwa magana?" Basu amsa masa ba. **93.** Saiya kafu a kansu duka da hannun dama da ƙarfi ya karyata.
94. Suka gabato izuwa gareshi suna gaggawa. (Sai sukace dashi mu muna bauta mata kai kana karyata)?. **95.** Sai yace (Dasu yana mai urustawa) "donme kuke bautawa abinda kuke sassaKawa a kan sune gumaka gareku). **96.** Allah ne ya halicce kuda abinda kuke bautawa (donme kuke bautawa abinda kuka assaƙa na gumaka? Ku bauta masa shi ƙadai). **97.** Sukace, "ku gina masa gini", (suka cika shi da itatuwa, suka hura masa wuta, sai gashi yana ci balbal), sai suka jefa shi a cikin wannan wuta mai tsananin zafi.
98. Sai suka nufi kaidi dashi, (wato jefa shi a wuta donta halakar dashi muka sanya su ababan ƙasƙastawa (wato ababan rinjaye yafice sumul daga cikin wutar).
99. Yace, "ni mai tafiya ne izuwa Ubangijina (daga gidan kafirci), da sannu Ubangijina zai shirye ni (izuwa indaya umarce ni in je, Shine Sham", samanin dayazo izuwa ƙasa abar tsarkakewa). **100.** Sai yace, "Ubangiji bani da daga salihai".
101. Sai mukayi masa albishir ɗa yaro mai yawan haƙuri.
102. A zamanin daya isa aiki a tare dashi (Ance ya kai ɗan shekara bakwai (7) Ance sha uku (13) sai yace "Ya kai dha yarona, haƙiƙa ni na gani a mafarki cewa ina yanka ka, (mafarkin Annabawa ko gaskiya ne, ayyukansu kuma da umarnin Allah ne, yace) "Ka duba mana, me ka gani (ga shawara, donya dcbe masa haso ga yanka ya juyo izuwa umarnin Allah), sai yace "ya Baba aikata abinda aka umarceka, da sannu zaka same ni cikin masu haƙuri (a kan wannan) in Allah ya yarda. **103.** A zamanin da suka miƙa wuyaya bugar dashi ƙasa izuwa goshinsa (kowane mutum yana da gefen goshi biyu, wannan abu ya afkune a Mina ya shara wuƙa kan maƙogwaronsa ba tayi masa komai ba, saboda wani abu mai tsarewa na daga ikon Allah). **104.** Muka kirawo shiya Ibrahimu. **105.** Lallai ka gasgata makarfi (da abin ka ƙoƙartayi na daga al'amarin yanka, to wannan ya isa). Haƙiƙa haka nan muke sa-kawa masu kyakkyawan aiki (da bin umarni mu yaye musu tsanani).
106. Haƙiƙa wannan yanka da akayi umarni dashi lallai Shine bala'i mabayyani.
107. Muka fanshe shi (abin umarni dayankawan nan Shine Ismailu ko Ishaƙu) da rago mai girma (na Aljanna, Shine wanda Habi-lu yakusantashi, Jibrilu yazo dashi Alihissalamu, sai Annabi Ibrahimu ya yanka shi yana mai cewa "Allahu akbar)".
108. Muka bar masa kyakkyawan yabo a cikin mutanen ƙarshe (har izuwa tashin alƙiyama). **109.** Gaisuwa daga garemu zuwa Annabi Ibrahimu (Alaihissalamu).
110. Kamar irin wannan sakamako ne muke sakawa masu kyakkyawan aiki.
111. Haƙiƙa shi yana daga bayinmu masu cikakken imani. **112.** Munyi masa albishir da Ishaƙa, (wato wannan ya nuna cewa Annabi Ishaƙa bashine abin yankawa ba) halin kasancewarsa Annabi daga cikin managarta. **113.** Mukayi albarka gareshi (da yawan zurriya), mukayi albarkabisa Ishaƙa. (muka sanya yawancin Annabawa daga 'ya'yansa)daga zurriyarsa, akwai daga zurriyarsa mai kyautatawa da mai zalintar kansa kafiri mabayyanin katirci.

(WANI ABU DAGA KISSAR ANNABI MUSA DA HARUNU ALHIMASSALAMU)

114. Haƙiƙa munyi baiwa bisa an-nabi Musa da Haruna (da An-nabci).
115. Mun tserar dasu da mutanensu (bani Isra'ila) daga bakin ciki mai girma, (wato bautar da Fir,aunu yake sa su

وَنَصَرْنَٰهُمْ فَكَانُواْ هُمُ الْغَٰلِبِينَ ﴿116﴾ وَءَاتَيْنَٰهُمَا الْكِتَٰبَ الْمُسْتَبِينَ ﴿117﴾
وَهَدَيْنَٰهُمَا الصِّرَٰطَ الْمُسْتَقِيمَ ﴿118﴾ وَتَرَكْنَا عَلَيْهِمَا فِي الْآخِرِينَ ﴿119﴾
سَلَٰمٌ عَلَىٰ مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ ﴿120﴾ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجْزِي الْمُحْسِنِينَ ﴿121﴾
إِنَّهُمَا مِنْ عِبَادِنَا الْمُؤْمِنِينَ ﴿122﴾ وَإِنَّ إِلْيَاسَ لَمِنَ الْمُرْسَلِينَ ﴿123﴾
إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِۦٓ أَلَا تَتَّقُونَ ﴿124﴾ أَتَدْعُونَ بَعْلًا وَتَذَرُونَ أَحْسَنَ
الْخَٰلِقِينَ ﴿125﴾ اللَّهُ رَبُّكُمْ وَرَبُّ ءَابَآئِكُمُ الْأَوَّلِينَ ﴿126﴾
فَكَذَّبُوهُ فَإِنَّهُمْ لَمُحْضَرُونَ ﴿127﴾ إِلَّا عِبَادَ اللَّهِ الْمُخْلَصِينَ ﴿128﴾
وَتَرَكْنَا عَلَيْهِ فِي الْآخِرِينَ ﴿129﴾ سَلَٰمٌ عَلَىٰ ءَالِ يَاسِينَ ﴿130﴾
إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجْزِي الْمُحْسِنِينَ ﴿131﴾ إِنَّهُۥ مِنْ عِبَادِنَا الْمُؤْمِنِينَ ﴿132﴾
وَإِنَّ لُوطًا لَّمِنَ الْمُرْسَلِينَ ﴿133﴾ إِذْ نَجَّيْنَٰهُ وَأَهْلَهُۥٓ أَجْمَعِينَ ﴿134﴾
إِلَّا عَجُوزًا فِي الْغَٰبِرِينَ ﴿135﴾ ثُمَّ دَمَّرْنَا الْآخَرِينَ ﴿136﴾
وَإِنَّكُمْ لَتَمُرُّونَ عَلَيْهِم مُّصْبِحِينَ ﴿137﴾ وَبِالَّيْلِ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿138﴾
وَإِنَّ يُونُسَ لَمِنَ الْمُرْسَلِينَ ﴿139﴾ إِذْ أَبَقَ إِلَى الْفُلْكِ الْمَشْحُونِ ﴿140﴾
فَسَاهَمَ فَكَانَ مِنَ الْمُدْحَضِينَ ﴿141﴾ فَالْتَقَمَهُ الْحُوتُ وَهُوَ مُلِيمٌ ﴿142﴾
فَلَوْلَا أَنَّهُۥ كَانَ مِنَ الْمُسَبِّحِينَ ﴿143﴾ لَلَبِثَ فِي بَطْنِهِۦٓ إِلَىٰ يَوْمِ يُبْعَثُونَ ﴿144﴾

116. Mun taimake su (a kan Kibɗawa) suka zama sune masu rinjaye.
117. Mun basu littafi mai isa matuka a cikakken bayani (cikin abinda yazo dashi a cikin had-dodi da hukunce-hukence da waninsune Attaura).
118. Mun shirye tafarki madaidaici.
119. Mun bar kyakkyawan yabo a garesu cikin mutanen karshe (har tashin alƙiyama).
120. Gaisuwa (daga garemu) a bisa Annabi Musa da Haruna .
121. Haƙiƙa mu kamar yadda muka saka musu, muke sakawa masa-na Ubangiji a matsayin Ihsani.
122. Haƙiƙa su suna daga bayin mu miminai.

(WANI ABU DAGA KISSAR ANNABI ILIYASU ALAIHISSALMU)

123. Haƙiƙa Annabi Iliyasu shi yana daga cikin manzanni (shi da zurriyar Haruna ɗan uwan Annabi Musa. An aiko shi izuwa mutanen Ba'alabakkah da nahiyoyinta).
124. Zamanin dayace da jama'arsa, "Shin ba kwa ji tsoron Ubangijinku ba?".
125. "Donme kuke bauta masa kuke barin mafi gwanintar talikai masu surantawa.
126. Allah ne Ubangijinku Ubangijin iyayen ku na farko.
127. Suka ƙaryatashi, haƙiƙa su ababan shigarwa ne (cikin wuta).
128. Sai bayin Allah ababan tsarkakewa (masu tsarkake aiki don Allah daga cikinsu to su sun tsira daga gareta).
129. Mun bar kyakkyawan yabo a gareshi cikin mutane (har izuwa tashin alƙiyama).
130. Gaisuwa daga garemu a bisa Iliyasu.
131. Haƙiƙa mu kamar wancanenka ne muke sakawa masu sanin Ubangiji a matsayin Ihsani.
132. Haƙiƙa shi yana daga cikin bayinmu muminai.

(WANI ABU DAGA CIKIN ƘISSAR ANNABI LUƊU ALAIHISSALAMU)

133. Haƙiƙa Annabi Luɗu yana daga cikin Manzannin Allah.
134. Zamanin da muka tsera dashi da iyalinsa baki ɗaya.
135. Sai gyatuma wacce take cikin masu wanzuwa (cikin azaba).
136. Sannan muka halakar da ragowar mutanensa.
137. Haƙiƙa ku kuna wucewa a kansu (a garesu a kan guraban su da gidaddajinsu cikin tafiye-tafiyen-ku), lokacin asuba.
138. Kuna wuce su da daddare, shin to ba kwa hankalci (abinda ya sauka akansu ba? Wato ku wa'azantu dashi)?.

(WANI ABU DAGA LABARIN ANNABI YUNUSA ALAIHISSALAMU)

139. Haƙiƙa Annabi Iliyasu yana daga cikin mazannin Ubangiji.
140. Zamanin daya izuwajirgi abin cikawa da halitta (zamanin dayayi fusaceceniya da mutanensa, zamanin da azaba bata sauka garesu ba, waddayayi musu alwashi da ita. To saiya hau jirgin saita tsaya dashi. Sai suka.ce, "akwai bawa daya gujewa ubangijinsa a nan)".
141. Sai yayi Kurri'a (da mutanen jirgi) ya zama daga cikin ababan rinjaya da ƙuri'a, (sai suka tsunduma shi a cikin kogi).
142. Sai kifi ya haɗiye shi alhali shi yazoda abindaza a zarge shi (Shine tafiyarsa izuwa kogi dashigarsa cikin jirgi bada izinin ubangijinsa ba).
143. Ba don cewa shiya kasance daga masu yanan tasbili ba, (wato masu ambaton Allah da yawa a cikin kifi, da faɗin LA ILAHA ILLA ANTA har izuwa ƙarshenta.
144. Daya zauna a cikin kifi izuwa ranar daza a tashi alƙiyama.
145. Sai muka jefar dashi (daga cikin kifi) a ƙasa faƙo, (a wannan ranar daya hadiye shi da walaha ya jeho shi dayammaci, Ance bayan kwana uku, Ance bayan kwana bakwai, Ance wanin waɗannan) alhali shi yana marar lafiya (kamar figaggen ɗan tsako).
146. Muka tsiro masa da itaciya ta duma (tanayi masa inuwa da maƙyengyamarta a bisa sabanin al'ada a cikin duma mu'ujuza ce gareshi, kuma bunsumn rema tana zuwa masa safiya dayammaci yana sha daga nononta har yayi ƙarfi).

حزب

* فَنَبَذْنَٰهُ بِالْعَرَآءِ وَهُوَ سَقِيمٌ ﴿145﴾ وَأَنۢبَتْنَا عَلَيْهِ شَجَرَةً مِّن يَقْطِينٍ ﴿146﴾ وَأَرْسَلْنَٰهُ
إِلَىٰ مِاْئَةِ أَلْفٍ اَوْ يَزِيدُونَ ﴿147﴾ فَـَٔامَنُواْ فَمَتَّعْنَٰهُمْ إِلَىٰ حِينٍ ﴿148﴾ فَاسْتَفْتِهِمُۥٓ أَلِرَبِّكَ
اَلْبَنَٰتُ وَلَهُمُ الْبَنُونَ ﴿149﴾ أَمْ خَلَقْنَا الْمَلَٰٓئِكَةَ إِنَٰثاً وَهُمْ شَٰهِدُونَ ﴿150﴾ أَلَآ إِنَّهُم مِّنِ
اِفْكِهِمْ لَيَقُولُونَ ﴿151﴾ وَلَدَ اللَّهُ وَإِنَّهُمْ لَكَٰذِبُونَ ﴿152﴾ أَصْطَفَى الْبَنَٰتِ عَلَى الْبَنِينَ ﴿153﴾
مَا لَكُمْ كَيْفَ تَحْكُمُونَ ﴿154﴾ أَفَلَا تَذَّكَّرُونَ ﴿155﴾ أَمْ لَكُمْ سُلْطَٰنٌ مُّبِينٌ ﴿156﴾ فَاتُواْ بِكِتَٰبِكُمُۥٓ
إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿157﴾ وَجَعَلُواْ بَيْنَهُۥ وَبَيْنَ الْجِنَّةِ نَسَباً وَلَقَدْ عَلِمَتِ الْجِنَّةُ إِنَّهُمْ لَمُحْضَرُونَ ﴿158﴾
سُبْحَٰنَ اللَّهِ عَمَّا يَصِفُونَ ﴿159﴾ إِلَّا عِبَادَ اللَّهِ الْمُخْلَصِينَ ﴿160﴾ فَإِنَّكُمْ وَمَا تَعْبُدُونَ ﴿161﴾
مَآ أَنتُمْ عَلَيْهِ بِفَٰتِنِينَ ﴿162﴾ إِلَّا مَنْ هُوَ صَالِ الْجَحِيمِ ﴿163﴾ وَمَا مِنَّآ إِلَّا لَهُۥ مَقَامٌ مَّعْلُومٌ ﴿164﴾
وَإِنَّا لَنَحْنُ الصَّآفُّونَ ﴿165﴾ وَإِنَّا لَنَحْنُ الْمُسَبِّحُونَ ﴿166﴾ وَإِن كَانُواْ لَيَقُولُونَ لَوَ اَنَّ
عِندَنَا ذِكْراً مِّنَ الْأَوَّلِينَ ﴿167﴾ لَكُنَّا عِبَادَ اللَّهِ الْمُخْلَصِينَ ﴿168﴾ فَكَفَرُواْ بِهِۦ
فَسَوْفَ يَعْلَمُونَ ﴿169﴾ وَلَقَدْ سَبَقَتْ كَلِمَتُنَا لِعِبَادِنَا الْمُرْسَلِينَ ﴿170﴾ إِنَّهُمْ لَهُمُ
الْمَنصُورُونَ ﴿171﴾ وَإِنَّ جُندَنَا لَهُمُ الْغَٰلِبُونَ ﴿172﴾ فَتَوَلَّ عَنْهُمْ حَتَّىٰ حِينٍ ﴿173﴾
وَأَبْصِرْهُمْ فَسَوْفَ يُبْصِرُونَ ﴿174﴾ أَفَبِعَذَابِنَا يَسْتَعْجِلُونَ ﴿175﴾ فَإِذَا نَزَلَ بِسَاحَتِهِمْ
فَسَآءَ صَبَاحُ الْمُنذَرِينَ ﴿176﴾ وَتَوَلَّ عَنْهُمْ حَتَّىٰ حِينٍ ﴿177﴾ وَأَبْصِرْ فَسَوْفَ يُبْصِرُونَ ﴿178﴾
سُبْحَٰنَ رَبِّكَ رَبِّ الْعِزَّةِ عَمَّا يَصِفُونَ ﴿179﴾ وَسَلَٰمٌ عَلَى الْمُرْسَلِينَ ﴿180﴾ وَالْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ الْعَٰلَمِينَ ﴿181﴾

147. Muka aiko shi (bayan wannan izuwa mutanen ninawa daga ƙasar Mausilu) izuwa mutum Dubu ɗari (100,000) kai sun ƙaru a kan haka ma da ishirin (20) koda talatin (30) ko da saba'in (70) na dubu). **148.** suka bada gaskiya (dashi yayin ganin azaba), muka jiyar dasu daɗi izuwa ƙarewar ajalinsu (a cikinsa).

(MUNAƘASHAR MUSHURIKAI A CIKIN AƘIDODINSU)

149. Ka nemi labarin kafiran Makka (don umstawa ne garesu), Shin 'ya'ya mata ne ga Ubangijinka? (Saboda riyarsu Mala'iku 'ya'yan Allah ne) su ko maza ne ke garesu (suka kebantada mafi ɗaukaka). **150.** Bari! Yansu mun halicci Mala'iku mataye ne? Su suna ganin halittar mu (bare su faɗi haka?). **151.** To jama'a, haƙiƙa su saboda ƙaryarsu suna cewa. **152.** "Allah ya haili (saboda fadinsu Mala'iku 'ya'yan Allah ne"). Haƙiƙa su lallai maƙaryata ne su (a cikin wannan magana). **153.** Yaya zai fifita mata a kan maza? **154.** Me ya sameku? Yaye kuke hukunta (wannan hukunci ɓatacce?). **155.** Shin ba kwayi tunani ba? (Ku tabbatacewa Ubangiji abin tsar-kakewa ne ga buran ɗa). **156.** Bari! Shinkuna da wata bayya-nanniyar hujja ne (bisa wannan cewa Allah yana da ɗa?). **157.** To ku zoda littafinku (Attaura, ku nuna min wannan a cikinsa), inkun kasance magasgata (a cikin wannan magana). **158.** Su mushurikai sun sanya nasaba tsakanin Ubangiji ta'ala da tsakanin Mala'iku (Ance an ambaci Mala'iku aljannu saboda fakuwar su ga duban ido, nasabar da suka sanya wa Allah cewa Mala'iku 'ya'yan Allah ne). Haƙiƙa su Mala'ikun nan sunsan masu wannan magana, lallai ababan ruguntsumawa ne a wuta. **159.** Tsarki ya tabbatarwa Ubangiji ga buran danganta ɗa a gareshi. **160.** Sai bayin Allah ababan tsarkakewa. **161.** Haƙiƙa kuda abinda kuke bautawa (nagumaka). **162.** Ku ba masu fitinar kowa bane da wannan magana taku. **163.** Sai wanda yake shi mai shiga Jahannama ne. Mala'ika Jibrilu yace da ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wa sallama. **164.** "Babu wani daga cikin mu (mu Mala'iku) face yana da muƙami abin sani (a sammai, yana bau-tawa Allah a ciki bazai ketare shi ba). **165.** "Haƙiƙa lallai mune masu shirya sahun mun a cikin sallah. **166.** " Haƙiƙa lallai mune masu tsakakewa ga Allah ga buran abinda bai kamace shi ba". **167.** Haƙiƙa kafiran Makkah sun kasance suna cewa. "Shin ɗaya kace lallai muna da littafi a garemu". **168.** "Da mun kasance bayin Allah, masu tsarkakewa bauta gareshi". **169.** Suka kafirtada littafin da akazo musu dashi (Shine alƙur'ani, wanda yafi daukaka daga waɗancan shauran littattafan). Da sannu zasu ga ƙarshen kafircinsu.

(KARFAFA KUDURIN ANIYA)

170. Haƙiƙa kalmar mu da taimakon bayinmu manzanni (Shine fadinsu Lallai nine zan yi rinjaye ni da manzannina). **171.** (Ko kuma faɗinsa) " Haƙiƙa su lallai sune ababan taimako. **172.** " Haƙiƙa rundunar mu (na muminai) lallai sune masu rinjaye (ga kafirai ta wajen hujja da nasara a kansu a duniyakoda ba'alinsu baici nasara ba a du-niya, amma a lahira zai ci nasara)_**173.** Ka rabu dasu har izuwa lokacin (daza a umarce ka dayaƙinsu). **174.** Ka dube sa (zamanin da azabazata sauka a kansu), da sannu zasu ga (aƙibar kafircinsu, sai suka faɗa don izgili "yaushe ne saukar wannan azabar?"). **175.** (Sai Ubangiji yace don firgita su) "Shin yansu da azabar mu suke garaje?". **176.** "Idan azabar ya sauka a farfajiyarsu to tir da safiyar ababan yiwa gargadi". **177.** Ka rabu dasu har izuwa wani lokaci. **178.** Ka dubada kyau da sannu zasu ga abindazai samesu (firgitarwa ne garesu, kuma rarraShine ga ma'aikin Allah, Sallallahu alaihi wa sallama). (TAMBARIN IBADODI) **179.** Tsarki ya tabbatarwa Ubangijinka, Ubangijin buwaya(1) ga buran abinda suke shirkantawa na dangana ɗa gareshi. **180.** Gaisuwa (daga Ubangiji) ya tabbata ga Musalai, (wato manzanni masu iyad da Tauhidi da Shari'o'i izuwa bayi daga Allah subhanahu wa ta'ala. **181.** Godiya dayabo ya tabbata ga Allah Ubangiji talikai (a bisa taimakon manzanni da halakar da kafirai).

1) Tambarin Ibadodi da wazifofi, dukkan masu darika da wannan suke rufe wazifarsu, daga wannan sai a sallami jama'a. Abinda Sawi yace abin nufi'dasuBHANA RABBIKA izuwa ƙarshenta a dinga fadar wannan aya kada a rafkana ga buranta saboda abinda aka ruwaito daga Sayydina Ali Karramalla-hu wajhahu yace, "wanda yaso yayi awo da mudu mafi cika na lada ranar alƙiyama, to na ƙarshen maganarsa ya kasance SUB-HANA RABBIKA har izuwa ƙarshenta". An ruwaito ga Abi Sa'idil Khudri yace, "naji Ma'aikin Allah, Sallallahu alaihi wa salla-ma ba ɗaya ba, ba biyu ba yana cewa a ƙarshen sallah tasa da kuma lokacin daya juyo yana cewa SUBHANA RABBIKA RBBIL IZZATI har izuwa ƙarshe. Saboda haka sufaye suka sa wannan aya tambarin dasuke bugawa a ƙarshen zikiransu. -Sanajiy

سُورَةُ صٓ مَكِّيَّةٌ 38

وَهِيَ سِتٌّ وَثَمَانُونَ ءَايَةً 86

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

ثمن

* صٓ وَالْقُرْءَانِ ذِي الذِّكْرِ بَلِ الَّذِينَ كَفَرُواْ فِي عِزَّةٍ وَشِقَاقٍ ﴿1﴾ كَمْ أَهْلَكْنَا
مِن قَبْلِهِم مِّن قَرْنٍ فَنَادَواْ وَّلَاتَ حِينَ مَنَاصٍ ﴿2﴾ وَعَجِبُواْ أَن جَآءَهُم
مُّنذِرٌ مِّنْهُمْ وَقَالَ الْكَافِرُونَ هَٰذَا سَاحِرٌ كَذَّابٌ ﴿3﴾ أَجَعَلَ الْآلِهَةَ إِلَٰهًا وَاحِدًا
إِنَّ هَٰذَا لَشَيْءٌ عُجَابٌ ﴿4﴾ وَانطَلَقَ الْمَلَأُ مِنْهُمْ أَنِ امْشُواْ وَاصْبِرُواْ عَلَىٰ
ءَالِهَتِكُمْ إِنَّ هَٰذَا لَشَيْءٌ يُرَادُ ﴿5﴾ مَا سَمِعْنَا بِهَٰذَا فِي الْمِلَّةِ الْآخِرَةِ
إِنْ هَٰذَا إِلَّا اخْتِلَاقٌ ﴿6﴾ أَنُزِلَ عَلَيْهِ الذِّكْرُ مِن بَيْنِنَا بَلْ هُمْ فِي شَكٍّ
مِّن ذِكْرِي بَل لَّمَّا يَذُوقُواْ عَذَابِ ﴿7﴾ أَمْ عِندَهُمْ خَزَآئِنُ رَحْمَةِ رَبِّكَ
الْعَزِيزِ الْوَهَّابِ ﴿8﴾ أَمْ لَهُم مُّلْكُ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا فَلْيَرْتَقُواْ
فِي الْأَسْبَابِ ﴿9﴾ جُندٌ مَّا هُنَالِكَ مَهْزُومٌ مِّنَ الْأَحْزَابِ ﴿10﴾ كَذَّبَتْ قَبْلَهُمْ قَوْمُ
نُوحٍ وَعَادٌ وَفِرْعَوْنُ ذُو الْأَوْتَادِ ﴿11﴾ وَثَمُودُ وَقَوْمُ لُوطٍ وَأَصْحَٰبُ لَيْكَةَ أُوْلَٰٓئِكَ
الْأَحْزَابُ ﴿12﴾ إِن كُلٌّ إِلَّا كَذَّبَ الرُّسُلَ فَحَقَّ عِقَابِ ﴿13﴾ وَمَا يَنظُرُ هَٰٓؤُلَآءِ إِلَّا صَيْحَةً
وَاحِدَةً مَّا لَهَا مِن فَوَاقٍ ﴿14﴾ وَقَالُواْ رَبَّنَا عَجِّل لَّنَا قِطَّنَا قَبْلَ يَوْمِ الْحِسَابِ ﴿15﴾

Wannan Sarutu Dawuriu ce Alaihissalamu

A Makka aka. saukar da ita Aya Tamanin dashida ce (86)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a lahira a keɓe.

Ita Wannan sura taƙunshi Manufar Mushurukai da Raddi a garesu da ambaton Kissoshin Ba'alin Annabawa Wacce Take ƙarfafa wannan Ma'ana ballantana kissar Dawuriu dasulaimana da Ayubada kulawa da Mushurikai da Bayanin Halinsu Ranar Alƙiyama da Ambaton kissar Annabi Adamu Alai-hissalamu dasujadar Mala'iku a Gareshi.

(MUNAƘASHAR MUSHURIKAI A KAN AƘIDODINSU DA RADDI A KANSU).

1..Allahu a'alamu bi muradihi bi zalika, Ubangiji yayi rantsuwa da alƙur'ani ma'abocin ɗaukaka. (Jawabin rantsuwa, Wannan lamari bai kasance kamar yadda kafuran Makka suke faɗa, na daga ƙididdigar iyayen giji ba), to bari waɗanda suka kafirta suna cikin jin girma (ga buran imani) da jayayya (da saɓawa ga Annabi Sallallahu alaihi wa sallama).

2. Da yawa muka halakar na daga tsareku waɗanda suka wuce, sai suka nemi taimako yayin saukar azaba a garesu, wannan lokaci kuma ba lokacin hutu da tsira ne ba.

3. Suna mana ki cewa mai gargaɗi daga cikinsu yazo musu (yana tsoratar dasu wuta bayan tashin alƙiyama Shine manzon Allah Sallallahu alaihi wa salla-ma), sai kafirai sukace, "wannan matsafi ne makaryaci".

4. Shin yasanya iyayen giji su zama guda ɗaya? Saboda me, yaya ubangiji guda ɗaya zai yalwaci mutane dukansu yayin dayace dasu ku ce, "LA ILAHA ILLALLAHU" sukace ƙaƙa zai gama halıtta dukkansu tareda kasancewarsa guda ɗaya), haƙiƙa wannan abu ne mai ban mana ki.

5. Manyan mutane daga cikinsu sun tafi (daga gurin tattarar nasu, nan ga Abi Ɖalib da jinsu daga ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wa sallama a gurin mazaunin cewa ku ce, "LA ILAHA ILLALLAHU" sai ba'alinsu ya na cewa ba'ali), "ku tafi ku daure (kan bautar iyayen gijinku), haƙiƙa wannan (abin ambato na tauhidi), lallai abu ne da ake nufinsa (garemu).

6. Bamu taɓa jin irin wannan a cikin addinin Annabi Isa ba) wannan bai kasance basai ƙage.

7. Yansu a saukar da alƙur'ani gareshi (alhali bai kasance mafi ɗaukakarmu ba? Ubangiji yace) bari! Su suna cikin kokonto ne daga ambatona (wato wahayina da suka ƙaryatada abinda yazo dashi).

8. Bari! Har yanzu basu ɗanɗani azaba ba. Dasun ɗranɗane ta dasun gasgata Annabi Sallallahu alaihi wa sallama a cikin abinda yazo dashi) ko suna da taskokin rahamar Ubangijinka ne mabuwayi mai yawankyauta.

9. Koko mulkin sammai da ƙassaida abinda yake tsakaninsu yana hunnunsu ne, su hau a cikin sabubba (masu sada zu izuwa sama su zoda wahayi su keɓanci' wanda suka ga dama dashi).

10. Su runduna ne wulakantattu msbabbu daga mndunoni a ca-nenka, (a cikin ƙaryatawarsu gareka).

11. Mutanen Annabi Nuhu sun ƙaryata manzanni gabansu da Adu da Samadu da Fir'auna mai turaku (ya kasance yana kafa turaku hudu ya ɗaure hannayen wanda yayi fushi a gareshiya ɗaure hannayensa da ƙafofuwansa izuwa wuya yanayi musu azaba).

12. Samudawa sun ƙaryata dasu da mutanen Annabi Luɗu da mutanen Laikati (wato Itace runƙunƙa su ne.mutanen Annabi Sha'aibu alaihissalam), waɗancanen sune ƙungiyoyi.

13. Bako ɗaya daga cikinsu face ya ƙaryata manzanni (saboda cewa su idan suka ƙaryata daga cikinsu kamar sun ƙaryata dukkan su ne, domin kiran su guda ɗaya ne Itace kira izuwa tauhidi) sai azabata tabbata a garesu.

14. Kafiran Makka basa sauraro sai tsawa guda ɗaya (wato busa guda ɗaya, Itace ranar alƙiyama wacce zata saukar da azaba a garesu) babu komarwa a gareta (wato baza a komar da ita ba).

15. Sai sukace yayin da Fa AMMA MANU TIYA KITABAHU ta sauka sai sukace "Ya Ubangiji gaggauta mana da littafin (ayyukanmu garemu tun kafin ranar Alƙiyama. Sun faɗi wancanenka don izgili ne).

اصْبِرْ عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَاذْكُرْ عَبْدَنَا دَاوُودَ ذَا الْأَيْدِ إِنَّهُ أَوَّابٌ (16)
إِنَّا سَخَّرْنَا الْجِبَالَ مَعَهُ يُسَبِّحْنَ بِالْعَشِيِّ وَالْإِشْرَاقِ (17)
وَالطَّيْرَ مَحْشُورَةً كُلٌّ لَّهُ أَوَّابٌ (18) وَشَدَدْنَا مُلْكَهُ وَآتَيْنَاهُ
الْحِكْمَةَ وَفَصْلَ الْخِطَابِ (19) * وَهَلْ أَتَاكَ نَبَؤُا الْخَصْمِ إِذْ تَسَوَّرُوا ربع
الْمِحْرَابَ (20) إِذْ دَخَلُوا عَلَىٰ دَاوُودَ فَفَزِعَ مِنْهُمْ قَالُوا لَا تَخَفْ
خَصْمَانِ بَغَىٰ بَعْضُنَا عَلَىٰ بَعْضٍ فَاحْكُم بَيْنَنَا بِالْحَقِّ وَلَا تُشْطِطْ وَاهْدِنَا
إِلَىٰ سَوَاءِ الصِّرَاطِ (21) إِنَّ هَٰذَا أَخِي لَهُ تِسْعٌ وَتِسْعُونَ نَعْجَةً
وَلِيَ نَعْجَةٌ وَاحِدَةٌ فَقَالَ أَكْفِلْنِيهَا وَعَزَّنِي فِي الْخِطَابِ (22) قَالَ لَقَدْ
ظَلَمَكَ بِسُؤَالِ نَعْجَتِكَ إِلَىٰ نِعَاجِهِ وَإِنَّ كَثِيرًا مِّنَ الْخُلَطَاءِ لَيَبْغِي
بَعْضُهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ إِلَّا الَّذِينَ آمَنُوا وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ وَقَلِيلٌ مَّا هُمْ
وَظَنَّ دَاوُودُ أَنَّمَا فَتَنَّاهُ فَاسْتَغْفَرَ رَبَّهُ وَخَرَّ رَاكِعًا وَأَنَابَ * (23) سجدة
فَغَفَرْنَا لَهُ ذَٰلِكَ وَإِنَّ لَهُ عِندَنَا لَزُلْفَىٰ وَحُسْنَ مَآبٍ (24) يَا دَاوُودُ
إِنَّا جَعَلْنَاكَ خَلِيفَةً فِي الْأَرْضِ فَاحْكُم بَيْنَ النَّاسِ بِالْحَقِّ
وَلَا تَتَّبِعِ الْهَوَىٰ فَيُضِلَّكَ عَن سَبِيلِ اللَّهِ إِنَّ الَّذِينَ يَضِلُّونَ
عَن سَبِيلِ اللَّهِ لَهُمْ عَذَابٌ شَدِيدٌ بِمَا نَسُوا يَوْمَ الْحِسَابِ (25)

(KISSATU DAWURIU ALAIHISSALAMU)

16. Sai Ubangiji ta'ala yace "daure bisa abinda suke faɗa maka", (akwai ban tsoro ga kafirai da rarrashi ga ma'aikin Allah Sal-lallahu alaihi wa sallama). Ka ambaci bawanmu Annabi Dawuriu ma'abocin ƙarfi (cikin ibada, ya kasance yana a zumi yau yana sha gobe, yana kiyamullaili rabindare, yana bacci a sulusinsa yana tsaiwa a sulusinsa yana bacci a ukunniyarsa yana tashi a shidanniyarsa), haƙiƙa shi mai yawan komawa ne izu-wa yardar Allah.

(YIN ZIKIRI TAREDA AMSHI A TAFE KO A ZAUNE)

17. Haƙiƙa mu mun hore duwarwat-su tare dashi, suna yin tasbihi [1] lokacin sallar Lisha da lokacin hudowar rana, (wato yayin data hudo kuma ta isa matuƙar haskenta).
18. Mun hore tsuntsaye abar tarewa gareshi tana zikiri tare dashi (wato tana amsa masa abinda ya faɗa), kowane daga duwar-watsun nan mai komawa ne izuwa biyayyar Annabi Dawuriu (da wannan tasbihi wato zikiri).
19. Mun karfafa mulkinsa (da 'yan sanda ke nan da sojoji, mutum dubu talatin ne suke kiwon masallacin Annabi Dawuriu a kow-ane dare). Munbashi hikima da annabci da dacewa cikin al'amura da rababbe zance (wato bayani ke nan mai warkarwa a kowace manufa).
20. Shin labarin maƙaraya yazo maka? lokacin da suka ɓullo a cikin masallacinsa, (yayin da aka hana su shiga garesu saboda shagala da ibadarsa, sun zo masa ne a ranar da yake shagala da ibada to 'yan sandansa suka hana su shiga gareshi).
21. Zamanin da suka ɓullo bisa Annabi Dawuriu yafirgita daga garesu, sukace kada kaji tsoro (Ance Mala'ikune guda biyu sukazo bisa surar maƙaraya abin nan da aka ambata ya afku garesu bisa sigar ƙaddarawa don a faɗakar da Annabi Dawuriu a bisa abinda ya afku gareshi. Annabi dawuriu yana da macce ɗari daya babu, ya nemi matar mutumin da bashi da wata mace sai ɗaya [1] donya aureta, saiya aureta ya tara da ita), sha-shin mu yayi zalinci a kan shashe. Yi hukinci tsakanin mu da gaskiya kada kayi zalinci, ka shiryar da mu izuwa tafarki madaidaici.
22. Haƙiƙa wannan ɗan'uwana ne (a kan addinina sunansa Uriyah ɗan Hana, wazirinsu ne), yana da saniya casa'in da tara (99) (wato mace), ni kuwa ina da saniya ɗaya [2] yace, "bani rainonta", saiya rinjaye ni a cikin zawarcinta.
23. Sai Annabi Dawuriu yace, "lallai ya zalince ka (saboda saniyar ka daya tare izuwa shanunsa), Haƙiƙa yawanci daga abokan hulɗa ba'alinsu yana zalinci kan ba'ali sai waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru su kuwa kaɗan ne ƙwarai" (Sai Mala'ikun nan guda biyu suka ce, suna masu tashi izuwa sama, "mutumin yayi hukunci a kansa)", sai Annabi Dawuriu ya sakankance cewa lallai mun fi-tince Shine (da musibar ƙaunar wancanenka mace), saiya nemi gafarar Ubangijinsa ya faɗi yana mai sujada, yakoma izuwa Ubangiji.
24. Muka gafarta masa wancanenka (a duniya), to haƙiƙa yana da ƙarin alheri da kyakkyawar makoma a lahira.
25. Ya Dawuriu haƙiƙa mun sanya ka halifa a bayan ƙasa katsara al'amarin mutane, kayi hukunci ysakanin mutane da gaskiya, kada kabi son zuciyaya ɓatar dakai ga buran son Allah (wato dalilai masu shiryarwa a kan kaɗaitar shi. Haƙiƙa waɗanda suke ɓacewa ga buran hanyar Allah. azaba mai tsanani ta tabbata garesu saboda mancewarsu ranar sakamako.

1) Yusabbihna Sawi yace suna tasbihi ai da harshen magana suna tafiya tare dashi a cikin tafiya, Waɗannan Duwatsu da waɗannan tsuntsaye suna yin zikiri tare dashi wato suna yin zikiri da harshen magana suna ta-fiya tare dashi a cikin mauƙibi. -Sanajiy
2) Sunansa Uriyah dan Hana,wazirinsa ne saboda asiri babba, matar da ake fada Itace uwar Annabi Sulaimanu, kuma irin wannan halal ne wato, yin wannan zawarci a cikin aure halal ne a shari'arsa, wannan zargi kuma don daukakar alkadarinsa. saboda kyakkyawan ayyukan managarta, miyagun ayyukan maku-santa ne. -Sawi

وَمَا خَلَقْنَا السَّمَآءَ وَالْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا بَاطِلًا ذَٰلِكَ ظَنُّ الَّذِينَ
كَفَرُوا فَوَيْلٌ لِّلَّذِينَ كَفَرُوا مِنَ النَّارِ ﴿26﴾ أَمْ نَجْعَلُ الَّذِينَ ءَامَنُوا وَعَمِلُوا
الصَّٰلِحَٰتِ كَالْمُفْسِدِينَ فِي الْأَرْضِ أَمْ نَجْعَلُ الْمُتَّقِينَ كَالْفُجَّارِ ﴿27﴾
كِتَٰبٌ أَنزَلْنَٰهُ إِلَيْكَ مُبَٰرَكٌ لِّيَدَّبَّرُوا ءَايَٰتِهِ وَلِيَتَذَكَّرَ أُولُوا الْأَلْبَٰبِ ﴿28﴾
* وَوَهَبْنَا لِدَاوُودَ سُلَيْمَٰنَ نِعْمَ الْعَبْدُ إِنَّهُ أَوَّابٌ ﴿29﴾ إِذْ عُرِضَ ثمن
عَلَيْهِ بِالْعَشِيِّ الصَّٰفِنَٰتُ الْجِيَادُ ﴿30﴾ فَقَالَ إِنِّي أَحْبَبْتُ حُبَّ
الْخَيْرِ عَن ذِكْرِ رَبِّي حَتَّىٰ تَوَارَتْ بِالْحِجَابِ ﴿31﴾ رُدُّوهَا عَلَيَّ فَطَفِقَ
مَسْحًا بِالسُّوقِ وَالْأَعْنَاقِ ﴿32﴾ وَلَقَدْ فَتَنَّا سُلَيْمَٰنَ وَأَلْقَيْنَا عَلَىٰ كُرْسِيِّهِ
جَسَدًا ثُمَّ أَنَابَ ﴿33﴾ قَالَ رَبِّ اغْفِرْ لِي وَهَبْ لِي مُلْكًا لَّا يَنبَغِي لِأَحَدٍ
مِّنۢ بَعْدِيَ إِنَّكَ أَنتَ الْوَهَّابُ ﴿34﴾ فَسَخَّرْنَا لَهُ الرِّيحَ تَجْرِي بِأَمْرِهِ
رُخَآءً حَيْثُ أَصَابَ ﴿35﴾ وَالشَّيَٰطِينَ كُلَّ بَنَّآءٍ وَغَوَّاصٍ ﴿36﴾ وَءَاخَرِينَ
مُقَرَّنِينَ فِي الْأَصْفَادِ ﴿37﴾ هَٰذَا عَطَآؤُنَا فَامْنُنْ أَوْ أَمْسِكْ بِغَيْرِ
حِسَابٍ ﴿38﴾ وَإِنَّ لَهُ عِندَنَا لَزُلْفَىٰ وَحُسْنَ مَـَٔابٍ ﴿39﴾ وَاذْكُرْ
عَبْدَنَا أَيُّوبَ إِذْ نَادَىٰ رَبَّهُ أَنِّي مَسَّنِيَ الشَّيْطَٰنُ بِنُصْبٍ وَعَذَابٍ ﴿40﴾
ارْكُضْ بِرِجْلِكَ هَٰذَا مُغْتَسَلٌ بَارِدٌ وَشَرَابٌ ﴿41﴾

(WANI ABU DAGA SAKAMAKO DA AZABA).

26. Bamu halicci sammai da ƙassaida abinda yake tsakanin su don wasa ba, wancanenka, (halittar abinda aka ambata don wasa) zaton waɗanda suka kafirta ne, to zaza na wuta ya tabbata ga waɗanda suka kafirta.

27. Bari! ma sanya waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru kamar maɓarnata cikin ƙasa? Bari ma sanya waɗanda suke tsoron Allah kamar fajirai (A'a wannan aya ta sauka ne zamanin da kafiran Makkah sukace da muminai su za a basu misalin abinda aka ba wa muminai).

28. Wannan littafi ne da muka saukar gareka mai albarka domin su lura da ayoyinsa, (su bada gaskiya), kuma don ma'abota hankula su wa'azantu.

(KISSAR ANNABI SULAIMANU ALAIHISSALAMU)

29. Mun ba wa Annabi Dawudasulaimanu, (wato daga matan nan daya karɓa daga wazirinza Uriyah a wannan lokaci yana dan shekara saba'in) MADALLA Babban bawa Sulaimanu, haƙiƙa shi mai komawa ne (cikin tasbihi da zikiri izuwa Allah cikin dukkan lokatansa).

30. Zamanin da akabijirar masa da dawakai masu tsaiwa kan wasu ukuda tsaida ɗaya a kan gefen kofato, ingarmu, (wato tana tsayawa in an nufi ta tsaya, in kuma an nufu sukuwa ta tsere, guda dubu ce, akabijirar masa, bayan ya sallaci azahar, saboda nufin zaiyi yaƙi a kanta na kafirai, yayin da akabijirar da ita ta kai ɗari tara (900) sai rana ta faɗi bai kasance yayi sallar La'asar basaboda haka).

31. Sai yace, " Haƙiƙa na so dawakai ga buran anɓaton Ubangijina, (wato sallar La'asar har tafaku ga shamaki (ga abinda yake tsareta ga buran idanuwa).

32. Ku koma da ita a gareni (waɗanda akabijirar masa, aka komo masa da ita, ya haɗu yana sharbewa (da kansakalinsa) sharɓewa, yana yanke wuyayunta (don neman kusanta izuwa Allah ta'ala, saboda ya shagala da ita ga buran sallah yayi sadaka da naman nata, wannan ya nuna halaccin naman dawakan a gareshi a shari'arsa. Sai Allah ya misanya masa daga gareta, mafi gaggawa ltace iska, tana gudu da umaminsa inda duk ya nufa).

33. Haƙiƙa mun jarrabi Annabi Sulaimana (da tuɓewar mulkinsa saboda faɗinsa zan kewayo a wannan dare bisa mace casa'in wanda yazo a cikin sahihaini na hadisin Abi Huraira radiyallahu anhu, yace, "Ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wa sallama yace, "Sulaimanu yace "Zan ke-wayo a wannan dare bisa mace casa'in ko ɗari dukkansu su zoda barde wandazai jihadi a cikin inganta addinin Allah, sai wazirinsa Uriyah yace dashi", ce ne in-sha-Allahu bai", sai ce "in - sha - Allahu ba" sai baki ɗayaba wacce tayi ciki sai mace ɗaya, saitazo ta rabin mutum, na rantse da Allah wanda raina yake ikonsa dayace, "inshaAllahu", dasun yi jihadi dukkansu suna barade baki ɗaya) Mun jefa jiki a kan gadonsa, (Shine rabin mutum ɗin nan wanda matarsa ta haifa sannan aka jarrabe shi da wannan yakoma izuwa Allah[1].

34. Yace "Ubangijina! kai gafara gareni, kuma ka bani mulki wanda bazai kasance ga ɗaya a bayana ba. Haƙiƙa kai, kaine mai yawan baiwa Ya Ubangiji!, haƙiƙa kai, kaine mai yawan kyauta".

35. Sai muka hore masa iska tana gudana da umaminsa tana mai taushi inda duk yanufa.

36. Muka hore masa shaiɗanu dukkan gwanin gini (da yake ginegine masu ban mana ki), da mai yawan nutso cikin kogi (don yafito masa da Lu'u-Lu'u).

37. Da waɗansu kuma ababan ɗaurewa a cikin mamruwa.

38. Wannan kyautar mu ce, kayi baiwa daga gareta (ga wandaka ga dama) ko ka riƙe babu Hisabi (a kanka cikin yin haka).

39. Haƙiƙa yana da kusanci nan garemu da kyan makoma.

(KISSAR ANNABI AYUBA ALAIHISSALAMU)

40. Ambaci bawanmu Annabi Ayuba, a zamanin daya kira Ubangijinsa, haƙiƙa ni Shaiɗan ya shafe ni da tsanani da raɗaɗi, (ya dangana wannan aiki izuwa Shaiɗan ko da yake abubuwa dukkansu daga Allah suke, don ladabi tareda Allah).

1)A nan mun bar abinda Shelu Mahalli yace cikin tafsirinsa, saboda rashin ingancin-sa wannan yana daga hadisaina Rarya, wanda malaman ta.rihi suka girbana hdrya. -Sanajiy •

وَوَهَبْنَا لَهُۥٓ أَهْلَهُۥ وَمِثْلَهُم مَّعَهُمْ رَحْمَةً مِّنَّا وَذِكْرَىٰ لِأُوْلِى
ٱلْأَلْبَٰبِ ﴿42﴾ وَخُذْ بِيَدِكَ ضِغْثًا فَٱضْرِب بِّهِۦ وَلَا تَحْنَثْ
إِنَّا وَجَدْنَٰهُ صَابِرًا نِّعْمَ ٱلْعَبْدُ إِنَّهُۥٓ أَوَّابٌ ﴿43﴾ وَٱذْكُرْ عِبَٰدَنَآ
إِبْرَٰهِيمَ وَإِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ أُوْلِى ٱلْأَيْدِى وَٱلْأَبْصَٰرِ ﴿44﴾ إِنَّآ أَخْلَصْنَٰهُم
بِخَالِصَةٍ ذِكْرَى ٱلدَّارِ ﴿45﴾ وَإِنَّهُمْ عِندَنَا لَمِنَ ٱلْمُصْطَفَيْنَ
ٱلْأَخْيَارِ ﴿46﴾ وَٱذْكُرْ إِسْمَٰعِيلَ وَٱلْيَسَعَ وَذَا ٱلْكِفْلِ وَكُلٌّ مِّنَ
ٱلْأَخْيَارِ ﴿47﴾ هَٰذَا ذِكْرٌ وَإِنَّ لِلْمُتَّقِينَ لَحُسْنَ مَـَٔابٍ ﴿48﴾ جَنَّٰتِ عَدْنٍ
مُّفَتَّحَةً لَّهُمُ ٱلْأَبْوَٰبُ ﴿49﴾ مُتَّكِـِٔينَ فِيهَا يَدْعُونَ فِيهَا بِفَٰكِهَةٍ
كَثِيرَةٍ وَشَرَابٍ ﴿50﴾ * وَعِندَهُمْ قَٰصِرَٰتُ ٱلطَّرْفِ أَتْرَابٌ ﴿51﴾ ربع
هَٰذَا مَا تُوعَدُونَ لِيَوْمِ ٱلْحِسَابِ ﴿52﴾ إِنَّ هَٰذَا لَرِزْقُنَا مَا لَهُۥ مِن نَّفَادٍ ﴿53﴾
هَٰذَا وَإِنَّ لِلطَّٰغِينَ لَشَرَّ مَـَٔابٍ ﴿54﴾ جَهَنَّمَ يَصْلَوْنَهَا فَبِئْسَ ٱلْمِهَادُ ﴿55﴾
هَٰذَا فَلْيَذُوقُوهُ حَمِيمٌ وَغَسَّاقٌ ﴿56﴾ وَءَاخَرُ مِن شَكْلِهِۦٓ أَزْوَٰجٌ ﴿57﴾
هَٰذَا فَوْجٌ مُّقْتَحِمٌ مَّعَكُمْ لَا مَرْحَبًۢا بِهِمْ إِنَّهُمْ صَالُوا۟ ٱلنَّارِ ﴿58﴾
قَالُوا۟ بَلْ أَنتُمْ لَا مَرْحَبًۢا بِكُمْ أَنتُمْ قَدَّمْتُمُوهُ لَنَا فَبِئْسَ ٱلْقَرَارُ ﴿59﴾
قَالُوا۟ رَبَّنَا مَن قَدَّمَ لَنَا هَٰذَا فَزِدْهُ عَذَابًا ضِعْفًا فِى ٱلنَّارِ ﴿60﴾

41. Akace dashi, "doki ƙasa da sawun ka (ya doke ta, sai idaniyar ruwa ta ɓulɓulo, sai aka ce) wannan ruwa ne (daza kayi wanka dashi) mai sanyi, kuma da ruwan sha (da zaka sha daga gareshi, sai yayi wanka da ruwan wannan idaniya, ya sha daga gareshi, sai dukkan cutada take zahirinsa da baɗinsa ta kau).

42. Muka bashi iyalinsa da misalinsu tare dasu (wato Allah ya raya masa 'ya'yansa waɗanda suka mutu kuma ya azurta masa misalinsu, daga misalinsu aka ƙara a cikin ƙuruciyarta,sannan matar Ramatu 'yar Afrasinu wato ɗan .Annabi Yusifu an ce, "sunanta Laiya 'yar Annabi Ya'akubu") don rahama daga garemu da gargaɗi ga ma'abota hankula.

43. Ka riƙi danƙin ciyawa da hannunka ka doki matar ka dashi (alhali ya rantse zai doke ta duka ɗari, (saboda tayi jinkiri a gareshi wata rana), kada kayi ƙari (ga buran dukan ta, saiya riƙi ɗari na daga Itacen tsaure ko waninsa ya doke ta dashi suka ɗaya. Haƙiƙa mun bayyana haƙurinsa ga mutane, madalla babban Bawa Ayuba[1]. Haƙiƙa shi mai yawan komawa ne izuwa Ubangijinsa.

(KISSAR ANNABI IBRAHIMU DA 'YA'YAYENSA)

44. Ambaci bayinmu Ibrahimu da Ishaƙu (ɗa ga Yaƙubu) ma'abota ƙarfi (a cikin bautar Allah) da basira (a cikin addini).

45. Haƙiƙa mun tsarkakesu da faɗa tatacciya (Itace tuna gidan lahira da aiki saboda ita).

46. Haƙiƙa su a gunmmu suna cikin abin zaɓi nagartattu.

47. Ka ambaci Annabi Isma'ila da Annabi Yusufu (wato Yasa'u ɗan Akhɗubu ɗan Ajuzu, Annabi Iliyasu Ya sanyashi halifa bisa bani Isra'ila sannan Allah ya an-nabtar dashi a kansu) da Zilƙifli, (an saɓa a cikin annabcinsa, Hakimu ya ruwaito daga Wahabu cewa Allah ya aiko bayan Annabi Ayubaya aiko ɗansa sunansa Bishru laƙabinsa Zalƙifli saboda ya raini Annabawa ɗari da suka gudu izuwa gareshi don gudun kisa, Ance kuma saboda ya lamunce da azumin rana da tsaiwar dare zaiyi hukunci tsakanin mutane ba tare dayayi fushi baya cika da abinda ya dauƙa). Kowane ɗay daga cikinsu yana cikin managarta[2].

48. Wannan kirari ne kyakkyawa garesu anan, haƙiƙa masu jin tsoron Allah suna da kyakkyawar makoma a lahira.

49. Aljannatai na zama abar budewar ƙofofi ce a garesu.

50. Masu dogaro (a kan gadaje masu jingina a cikinta (a kan gadaje) suna kira a cikintada abin marmari mai yawa da abin sha, (ba a cin abinci don yunwa a cikin aljanna).

51. Matayc masu tsarc idanuwansu suna garcsu tsareku, (shekarunsu ɗaya Shinc talatin da ukuuku).

52. Wannan abin ambato Shine abinda ake muku alwashi dashi (a gaibu) saboda ranar sakamako.

53. Haƙiƙa wannan lallai arzikin mune ba ƙarewa gareshi.

(HUSUMAR 'YAN WUTA ALLAH YA KIYASHEMU)

54. Wannan (abinda aka ambatashine sakamakon muminai) kuma haƙiƙa mummunar makoma ta tabbata ga masu shishshigi.

55. Jahannama zasu shigeta, to tur shimfida.

56. Wannan azaba ruwan zafi na mai ƙonewa to su ɗanɗane shi, da mugunya ta 'yan wuta.

57. Da kuma wani (ruwan) na daga makamancinsa iri- iri (ana cewa zamanin shigar su wuta su da mabiyansu).

58. Wannan bindu ne (wato ƙungiyace) mai faɗawa wuta tare dasu (sai shiyagabanmu su ce), "ba maraba ga wannan ƙungiya, ai su masu kutsawa wuta ne".

59. (To sai mabiya su ce "a'a kune ba marabadaku ,ba, kune kuka gabatar da kafirci garemu (inji mabiyan) to tur da wannan mazauni namu da mu da ku".

60. Mabiyan har yau suka sake cewa "Ya Ubangijinmu wanda yagabatar da wannan a garemu to ƙara masa azaba abin ninkawa, (wato kamar azaba a wuta").

1) Amma a shari'armu bazai kubutarbasaiya do-keta sau darı wato dukansa da 'yan itatuwa a tattare, baza a Rirga ɗayagareta ba. -Sanajiy- 2) Mun ziyarce shi a garinsa da ake ce dashi Al-kifil, tsohon gari ne a hanyar ka izuwa Kufa, tsakanin Bagadaza da Ku-fa Malam ya ziyarce shi tareda jama'arsa, wato a kwaye dashi akwai Raburbura na manya-manyan mu-tanc masu zati mai tsawon fiyedana muta-nenmu na yau, Malam yana zaton waɗannan mutane suna daga cikin Annabawan daya raina wanda Shelu-Mahalli yake faɗa akwai kwarjini mai yanan gaske a wurin. -Sanajiy-

وَقَالُوا مَا لَنَا لَا نَرَىٰ رِجَالًا كُنَّا نَعُدُّهُم مِّنَ ٱلْأَشْرَارِ ﴿61﴾
أَتَّخَذْنَاهُمْ سُخْرِيًّا أَمْ زَاغَتْ عَنْهُمُ ٱلْأَبْصَارُ ﴿62﴾ إِنَّ ذَٰلِكَ لَحَقٌّ
تَخَاصُمُ أَهْلِ ٱلنَّارِ ﴿63﴾ قُلْ إِنَّمَا أَنَا مُنذِرٌ وَمَا مِنْ إِلَٰهٍ إِلَّا ٱللَّهُ
ٱلْوَاحِدُ ٱلْقَهَّارُ ﴿64﴾ رَبُّ ٱلسَّمَاوَاتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا ٱلْعَزِيزُ ٱلْغَفَّارُ ﴿65﴾
قُلْ هُوَ نَبَؤٌا عَظِيمٌ ﴿66﴾ أَنتُمْ عَنْهُ مُعْرِضُونَ ﴿67﴾ مَا كَانَ لِيَ مِنْ عِلْمٍ
بِالْمَلَإِ ٱلْأَعْلَىٰ إِذْ يَخْتَصِمُونَ ﴿68﴾ إِن يُوحَىٰ إِلَيَّ إِلَّا أَنَّمَا أَنَا نَذِيرٌ
مُّبِينٌ ﴿69﴾ إِذْ قَالَ رَبُّكَ لِلْمَلَٰٓئِكَةِ إِنِّي خَالِقٌ بَشَرًا مِّن طِينٍ ﴿70﴾
فَإِذَا سَوَّيْتُهُ وَنَفَخْتُ فِيهِ مِن رُّوحِي فَقَعُوا لَهُ سَاجِدِينَ ﴿71﴾ فَسَجَدَ
ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ كُلُّهُمْ أَجْمَعُونَ ﴿72﴾ إِلَّا إِبْلِيسَ ٱسْتَكْبَرَ وَكَانَ مِنَ ٱلْكَافِرِينَ ﴿73﴾
قَالَ يَا إِبْلِيسُ مَا مَنَعَكَ أَن تَسْجُدَ لِمَا خَلَقْتُ بِيَدَيَّ أَسْتَكْبَرْتَ
أَمْ كُنتَ مِنَ ٱلْعَالِينَ ﴿74﴾ قَالَ أَنَا خَيْرٌ مِّنْهُ خَلَقْتَنِي مِن نَّارٍ وَخَلَقْتَهُ
مِن طِينٍ ﴿75﴾ قَالَ فَاخْرُجْ مِنْهَا فَإِنَّكَ رَجِيمٌ ﴿76﴾ وَإِنَّ عَلَيْكَ لَعْنَتِيَ
إِلَىٰ يَوْمِ ٱلدِّينِ ﴿77﴾ قَالَ رَبِّ فَأَنظِرْنِي إِلَىٰ يَوْمِ يُبْعَثُونَ ﴿78﴾ قَالَ
فَإِنَّكَ مِنَ ٱلْمُنظَرِينَ ﴿79﴾ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْوَقْتِ ٱلْمَعْلُومِ ﴿80﴾ قَالَ فَبِعِزَّتِكَ
لَأُغْوِيَنَّهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿81﴾ إِلَّا عِبَادَكَ مِنْهُمُ ٱلْمُخْلَصِينَ ﴿82﴾

61. Kafiran Makka suka ɗora cewa, (alhali su suna cikin wuta), Menene ya sa bamu ga mazaje da muka ƙirgasu a duniya daga ashararai ba?.
62. Shin mun riƙe su abin izgili dasune a duniyako kuwa idanu-wanmu sun karkace ga buran su bamu gan su ba, (kamar Ammaru da Bilalu dasuhaibu da Salmanu da sauran fuƙara'ul muslimina").
63. " Haƙiƙa wancanenka lallai wajibi ne ya afku, Shine husumar 'yanwuta".

(WANI ABU NA DALILAN AMSAR GASKIYAR MA'AIKIN ALLAH SALLALLAHU ALAIHIWA SALLAMA)

64. Gaya musu (Ya Annabi Sallallahu alaika wa sallama) dahir ni mai gargaɗi ne (da wuta) kawai, ba abin bautawa da gaskiya sai Allah maɗayancin sarki, mai yawan rinjiye (ga halittarsa).
65. Ubangijin sammai da ƙassaida abinda yake tsakaninsu mai rinjaye (a kan al'amarinsa) mai yawan gafara (ga waliyansa).
66. Cene (dasu) "Shi alƙur'ani labari ne mai girma".
67. "Ku kuke bijirewa ga buransa. (Shi alƙur'ani wandana baku labari dashi yazo mukuda abinda ba a saninsa sai daga wahayi, wannan Shine faɗinsa).
68. "Bani da wani sani da jama'a mafi ɗaukaka (sune Mala'iku), zamanin dasuke yin husuma (a cikin sha'anin Annabi Adamu lokacin da Allah yace dasu, "Ni zan halifa a bayan ƙasan nan har izuwa ƙarshen maganar").
69. "Ba a aiko komai izuwa gareni basai cewa dahir dai ni mai gargaɗi ne mabayyanin gargaɗi (agarreku)".

(KISSAR HALITTAR MUTUM DA GIRMAMA WAR DA ALLAH YAYI MASA)

70. Ambaci yayin da Ubangijinka ya faɗa ga Mala'iku cewa haƙiƙa ni mai halittar mutumne daga yunɓu (Annabi Adamu).
71. Idan ne daidaitashi na gudanar da ran da yake a mallakata a cikinsa, ya zama mai rai, (liƙa rai izuwa Allah ɗaukakawa ne ga Annabi Adamu, shi rai jiki ne mai laushi, daShine mutum yake rayuwa), ku faɗi kuna masu sujada gareshi (wato sujada irin ta sunkuyar dakai ba ɗora goshi a ƙasa ba).
72. Sai Mala'iku sukayi sujada dukkansu.
73. Sai Iblis Shine uban aljannu yayi girman kai ya kasance daga cikin kafirai a cikin sanin Allah.
74. Ya Iblisu mai ya hanaka kayi sujada ga abinda na halittada ƙuduratada iradata, (wannan ɗukakawa ne ga Annabi Adamu, saboda kowane abin halitta;Allah ne yajiɓinci halittarsa), kayi girman kaine ga buran sujada a yanzu? Ko ka kasance daga maɗaukaka (na Mala'iku saboda kasancewarka daga cikinsu?).
75. Sai yace, "Ka halicce ni daga wuta, shi ko Ka halicce shi daga yunɓu".
76. Ubangiji yace, "fita daga cikinta, (wato Aljanna), haƙiƙa kai abin korewa ne daga rahama ta har abada".
77. Yace, "Ubangiji! ka saurarамin har izuwa ranar daza atashi mutane".
78. Sai yace. "Ubangiji Kabani Luka shi zuwa ranar lahira.
79. Ubangiji yace, "haƙiƙa kai kana cikin ababan yi wa sauraro".
80. "Izuwa rana abar sani"
81. Yace, "na rantse da girmanka lallai zan halakar dasu baki ɗaya ".
82. "Sai bayinka ababan tsarkakewa daga garesu".

ثمن

* قَالَ فَالْحَقُّ وَالْحَقَّ أَقُولُ ۝ لَأَمْلَأَنَّ جَهَنَّمَ مِنكَ وَمِمَّن تَبِعَكَ مِنْهُمْ
أَجْمَعِينَ ۝83 قُلْ مَا أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ مِنْ أَجْرٍ وَمَا أَنَا مِنَ الْمُتَكَلِّفِينَ ۝84
إِنْ هُوَ إِلَّا ذِكْرٌ لِّلْعَٰلَمِينَ ۝85 وَلَتَعْلَمُنَّ نَبَأَهُۥ بَعْدَ حِينٍ ۝86

39 سُورَةُ الزُّمَرِ مَكِّيَّة
وَهِيَ ثِنْتَانِ وَسَبْعُونَ ءَايَةً 72

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

تَنزِيلُ الْكِتَٰبِ مِنَ اللَّهِ الْعَزِيزِ الْحَكِيمِ ۝1 إِنَّا أَنزَلْنَا
إِلَيْكَ الْكِتَٰبَ بِالْحَقِّ فَاعْبُدِ اللَّهَ مُخْلِصًا لَّهُ الدِّينَ ۝2
أَلَا لِلَّهِ الدِّينُ الْخَالِصُ وَالَّذِينَ اتَّخَذُوا مِن دُونِهِۦ أَوْلِيَآءَ مَا نَعْبُدُهُمْ
إِلَّا لِيُقَرِّبُونَا إِلَى اللَّهِ زُلْفَىٰ إِنَّ اللَّهَ يَحْكُمُ بَيْنَهُمْ فِي مَا هُمْ فِيهِ
يَخْتَلِفُونَ ۝3 إِنَّ اللَّهَ لَا يَهْدِي مَنْ هُوَ كَٰذِبٌ كَفَّارٌ ۝4 لَّوْ أَرَادَ
اللَّهُ أَن يَتَّخِذَ وَلَدًا لَّاصْطَفَىٰ مِمَّا يَخْلُقُ مَا يَشَآءُ سُبْحَٰنَهُۥ
هُوَ اللَّهُ الْوَٰحِدُ الْقَهَّارُ ۝5 خَلَقَ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضَ بِالْحَقِّ يُكَوِّرُ
الَّيْلَ عَلَى النَّهَارِ وَيُكَوِّرُ النَّهَارَ عَلَى الَّيْلِ وَسَخَّرَ الشَّمْسَ وَالْقَمَرَ
كُلٌّ يَجْرِي لِأَجَلٍ مُّسَمًّى أَلَا هُوَ الْعَزِيزُ الْغَفَّٰرُ ۝6

83. Ubangiji yace, "ina tabbatar da gaskiya, gaskiya nake faɗa, lallai zan cika jahannama dakai da zurriyarka, daga kuma wanda yabika daga cikinsu baki ɗaya ".
84. Cene, "ni ban tambaye ku wani lada bisa aikena ba, ni ban kasance daga masu girbawa alƙur'ani ƙarya ba.
85. "Shi wannan alƙur'ani bai kasance basai gargadi ga mahankaltan mutane da aljannu ban da Mala'iku".
86. Wallahi lallai zaku san gaskiyar wannan labari, bayan wani lokaci (Shine Alƙiyama).

Wannan Suratu Zumari ce

A Makka aka saukar da ita Aya Saba'in da Biyu ce (72)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a lahira a keɓe.

ta Wannan Sura Ta Kunshi)Dalilan Girman Allah Da Ambaton Mumini Da Kafiri)a Taƙawa Da Ikhlasi Da Haske Da Buɗen Kirji Da Musalce-Musalce Acikin AIKur'ani Da Wanin Wannan Dasujadar Mala'ikuda Sama'a Ta Sufaye Dasuke Yi A Cikin Zikiri.

(DALILAN GIRMAN UBANGIJI)

1. Ubangiji yace saukarwar Alƙur'ani daga Allah ne gwaiii, mabuwayi a cikin mulkinsa.
2. . Haƙiƙa mu mun saukar da wannan littafi gareka da gaskiya, sai ka bautawa Allah kana mai tsarkakewar bauta a gareshi (daga shirka, wato mai kaɗaitashi).
3. Yaku jama'a, addini tatacce na Allah ne kaɗai, (ba wanda ya cancanceshi sai shi), waɗanda suka riƙi ababan soyayyaba Allah ba, (na daga gumaka sune kafiran Makka sukace) "Barna bauta musu sai donsu kusantamu izuwa Allah, kusantawa, haƙiƙa Ubangiji zaiyi hukunci tsakaninsu (da tsakanin musulmi) cikin abindasu suke sassaɓawa (a cikinsa na daga sha'anin al'amarin addini, ya shigar da muminai Aljanna kafirai kuma wuta).
4. Haƙiƙa Ubangiji bazai shiryi, wanda yake maƙaryaci (a cikin dangana ɗa izuwa gareshi), tsagaggen kafiri (da bautar wanin Allah, Allah bazai shirye shi ba).
5. . Da Allah yanufi ya riƙi ɗa, (tamfar da sukace ya riƙi ɗa ɗin nan), daya zaɓi abinda yaga dama, daga abinda ya halitta, (ya riƙe shi ɗan, ba waɗanda sukace Mala'iku 'ya'yan Allah ba, da Uzairu da Masihu). Tsarki ya tabbatarwa Ubangiji (ga buran riƙon ɗa), Shine Allah madayanci, marinjayi (ga halitta).
6. Ya halicci sammai da ƙassaida gaskiya, yana shigar da dare a kan rana (saiya ƙaru), yana shigar da rana a kan dare (sai dare ya ƙaru)[1] ya hore rana da wata, kowannen yana gudana a cikin falaƙinsa, izuwa ajali abin anbato (Shine alƙiyama). Shine mabuwayi (a kan al'amarinsa), mai yin azaba (ga magautansa), mai yawan gafara (ga masoyansa).

1) Sawi yace matukar wannan dai sa'a goma sha hudii (14), matukar tawaya sa'a goma (10), to Rarin nan sa'a hudu (4) ce take Raruwa, wani yayi ta kasance cikin dare, wani yayi ta ka-sance cikin rana. -Sawi-

خَلَقَكُم مِّن نَّفْسٖ وَٰحِدَةٖ ثُمَّ جَعَلَ مِنْهَا زَوْجَهَا وَأَنزَلَ
لَكُم مِّنَ اَلْأَنْعَٰمِ ثَمَٰنِيَةَ أَزْوَٰجٖ يَخْلُقُكُمْ فِي بُطُونِ
أُمَّهَٰتِكُمْ خَلْقاٗ مِّنۢ بَعْدِ خَلْقٖ فِي ظُلُمَٰتٖ ثَلَٰثٖ ذَٰلِكُمُ اُللَّهُ
رَبُّكُمْ لَهُ اُلْمُلْكُ لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَأَنَّىٰ تُصْرَفُونَ ٧ إِن تَكْفُرُواْ فَإِنَّ اَللَّهَ
غَنِيٌّ عَنكُمْ وَلَا يَرْضَىٰ لِعِبَادِهِ اِلْكُفْرَ وَإِن تَشْكُرُواْ يَرْضَهُ لَكُمْ
وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٞ وِزْرَ أُخْرَىٰ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُم مَّرْجِعُكُمْ فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ
تَعْمَلُونَ إِنَّهُۥ عَلِيمُۢ بِذَاتِ اِلصُّدُورِ ٨ ۞ وَإِذَا مَسَّ اَلْإِنسَٰنَ ضُرّٞ دَعَا ربع
رَبَّهُۥ مُنِيباً إِلَيْهِ ثُمَّ إِذَا خَوَّلَهُۥ نِعْمَةٗ مِّنْهُ نَسِيَ مَا كَانَ يَدْعُواْ إِلَيْهِ
مِن قَبْلُ وَجَعَلَ لِلَّهِ أَندَاداٗ لِّيُضِلَّ عَن سَبِيلِهِۦ قُلْ تَمَتَّعْ بِكُفْرِكَ
قَلِيلاً إِنَّكَ مِنْ أَصْحَٰبِ اِلنَّارِ ٩ أَمَنْ هُوَ قَٰنِتٌ ءَانَآءَ
اَلَّيْلِ سَاجِداٗ وَقَآئِماٗ يَحْذَرُ اُلْأٓخِرَةَ وَيَرْجُواْ رَحْمَةَ رَبِّهِۦ
قُلْ هَلْ يَسْتَوِے اِلذِينَ يَعْلَمُونَ وَالذِينَ لَا يَعْلَمُونَ
إِنَّمَا يَتَذَكَّرُ أُوْلُواْ اُلْأَلْبَٰبِ ١٠ قُلْ يَٰعِبَادِ اِلذِينَ ءَامَنُواْ اُتَّقُواْ
رَبَّكُمْ لِلذِينَ أَحْسَنُواْ فِي هَٰذِهِ اِلدُّنْيَا حَسَنَةٞ وَأَرْضُ اُللَّهِ وَٰسِعَةٌ
إِنَّمَا يُوَفَّى اَلصَّٰبِرُونَ أَجْرَهُم بِغَيْرِ حِسَابٖ ١١

7. Ya halicce ku daga kai guda ɗaya (Annabi Adamu), sannan ya halicci matar daga ita kan nasa (Itace Hauwa'u), ya saukar da nau'i takwas na daga dabbobi don ku (yace, "ya ambaci saukarwa saboda ita dabbobin nan ta kasantu da tsiri ne, shi kuma tsirin Shine abincinta, kuma shi tsirin ya kasantu daga ruwa abin saukarwa daga sama, kuma Ance an saukar dasune daga Aljanna izuwa ƙasa) nau'i takwas, (raƙuma, shanu, tumakai, awa-kai kowanne namiji da mace). Yana halittarku a cikin cikkunan iyayenku, halitta bayan halitta, (ɗigon ƙazanta, sannan gudan jini, sannan gudan tsoka) a cikin duffai guda uku, (duhun ciki, duhun mahaifa duhun riga) wancanenku Allah ke nan Ubangijinku, cikakken mulki na gareshi shi kaɗai ba abin bautawa da gaskiya sai shi. To yayakuke juyawa (ga buran bauta masa izuwa bautar waninsa).
8. Inkun karfirce to haƙiƙa Allah mawadaci ne ga buranku, baya yarda da kafirci daga bayinsa, (kodaya nuƒe shi daga ba'alinsu) Inkun godewa Allah, kuka bada gaskiya zai yarda da wannan godiyagareku. Wata kai bazata ɗauki nauyin wata kai badabam, sannan izuwa Ubangijinkune makomar ku, zai baku labari da abinda kuka kasance kuna aikatawa, haƙiƙa shi masanine da haluluwan zukatan bayi.

(MUMINI DA KAFIRI)

9. Idan tsanani ya sami kafiri saiya roƙi Ubangijinsa yana mai komar da al'amarinsa izuwa gareshi, sannan idan ya bashi ni'ima daga gareshi saiya mance kasancewarsa yana ƙanƙan dakai izuwa Allah tun gaba, sai yasanya gumaka ga Allah, donya ɓace ga buran bautawa Ubangijinsa, Cene, "ji dadi da kafircinka kaɗan (izuwa ƙarewar ajalinka), Haƙiƙa kai kana daga cikin 'yan wuta"
10. Shin yanzu wanda yake a tsaye da al,amarin Ubangiji a cikin sa'o'in dare, yana mai sujada ga, Allah yana tsaye a cikin sallah yana tsoron azabar lahira, yana ƙaunar Aljannar Ubangijinsa, zai zama (kamar mai saɓon Allah da kafirci da waninsa? A'a, bazai zama ba). Cene "Yalla waɗanda suke ma'abuta sani zasuyidaidai da waɗanda ba ma'abota sani ba? (A'a, bazasuyidaidai ba), dahir dai ma'abota hankula kaɗai sune suke wa'azantuwa.

(TAƘAWA DA IKHLASI DA NISANTAR WANIN ALLAH)

11. Ka faɗa, "Yaku bayina waɗanda suka bada gaskiyakuji tsoron Ubangijinku, aljanna ta tabbata ga waɗanda sukayi kyakykyawan aiki a wannan duniya, ƙasar Allah mayalwaciyace (kuyi hijira izuwa gareta wato wanda taƙawa ta wuyata gareshi a wani guri, to ya ƙaura izuwa wani gurin da taƙwar zata sauƙaƙa gareshi, don ba hanzari a cikin sakaci izuwa wannan, to wannan hijira wajiba ce, takan zama mandubiya, kamar idan yayi hijira daga ƙasa wacce ba nagargaru a cikinta, izuwa ƙasa wacce take akwai nagargaru dazai shiriya dasu, takan zama makumha kamar idan yayi hiJira izuwa ƙasa wacce nagargaru suke cikinta wato ma'abota ilimi da salaha izuwa ƙasa da ba malamai a cikinta ba nagargaru, takan zama haramun, kamar idan yayi hijira daga ƙasar daya amince da addininsa a cikinta izuwa ƙasar da bai amince da addinin ta ba, hukunci biyar ke nan dangane da hijira, Shaihu Usman Radiy-allahu yayi bayanin hijira a cikin littafinsa (Bayanil Wujubu Hijrati) kuyi hijira izuwa gareta (daga tsakanin kafirai da ganin ayyukan munkari). Dahir ɗai ana cikawa masu haƙuri ladansu bada lissafi ba.

قُلْ إِنِّيَ أُمِرْتُ أَنْ أَعْبُدَ اللَّهَ مُخْلِصًا لَّهُ الدِّينَ وَأُمِرْتُ لِأَنْ أَكُونَ أَوَّلَ
الْمُسْلِمِينَ ﴿12﴾ قُلْ إِنِّيَ أَخَافُ إِنْ عَصَيْتُ رَبِّي عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿13﴾
قُلِ اللَّهَ أَعْبُدُ مُخْلِصًا لَّهُ دِينِي فَاعْبُدُوا مَا شِئْتُم مِّن دُونِهِ
قُلْ إِنَّ الْخَاسِرِينَ الَّذِينَ خَسِرُوا أَنفُسَهُمْ وَأَهْلِيهِمْ يَوْمَ الْقِيَامَةِ أَلَا ذَٰلِكَ
هُوَ الْخُسْرَانُ الْمُبِينُ ﴿14﴾ لَهُم مِّن فَوْقِهِمْ ظُلَلٌ مِّنَ النَّارِ
وَمِن تَحْتِهِمْ ظُلَلٌ ذَٰلِكَ يُخَوِّفُ اللَّهُ بِهِ عِبَادَهُ يَا عِبَادِ فَاتَّقُونِ ﴿15﴾
وَالَّذِينَ اجْتَنَبُوا الطَّاغُوتَ أَن يَعْبُدُوهَا وَأَنَابُوا إِلَى اللَّهِ
لَهُمُ الْبُشْرَىٰ فَبَشِّرْ عِبَادِ الَّذِينَ يَسْتَمِعُونَ الْقَوْلَ فَيَتَّبِعُونَ أَحْسَنَهُ
أُولَٰئِكَ الَّذِينَ هَدَاهُمُ اللَّهُ وَأُولَٰئِكَ هُمْ أُولُوا الْأَلْبَابِ ﴿16﴾
ثمن
* أَفَمَنْ حَقَّ عَلَيْهِ كَلِمَةُ الْعَذَابِ أَفَأَنتَ تُنقِذُ مَن فِي النَّارِ ﴿17﴾
لَٰكِنِ الَّذِينَ اتَّقَوْا رَبَّهُمْ لَهُمْ غُرَفٌ مِّن فَوْقِهَا غُرَفٌ مَّبْنِيَّةٌ تَجْرِي مِن
تَحْتِهَا الْأَنْهَارُ ﴿18﴾ وَعْدَ اللَّهِ لَا يُخْلِفُ اللَّهُ الْمِيعَادَ ﴿19﴾ أَلَمْ تَرَ أَنَّ اللَّهَ
أَنزَلَ مِنَ السَّمَاءِ مَاءً فَسَلَكَهُ يَنَابِيعَ فِي الْأَرْضِ ثُمَّ
يُخْرِجُ بِهِ زَرْعًا مُّخْتَلِفًا أَلْوَانُهُ ثُمَّ يَهِيجُ فَتَرَاهُ مُصْفَرًّا
ثُمَّ يَجْعَلُهُ حُطَامًا إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَذِكْرَىٰ لِأُولِي الْأَلْبَابِ ﴿20﴾

12. Cene, "Haƙiƙa ni an umarce ni in bautawa Allah mai tsarkake-war addini a gareshi daga shir-ka, an umarce ni in kasance farkon Musulmi (na wannan al'umma)".

13. Cene, " Haƙiƙa ni ina jin tsoron azabar rana mai girma, in na saɓi Ubangijiha".

14. Cene, "Allah kaɗai nake bautawa ina mai tsarkake addinina (daga shirka) gareshi. Ku bau-tawa abinda kuka ga dama ba Allah ba (akwai ban tsoro cikinsa garesu da sanarwa cewa su bazasu bautawa Allah ba). Cene, " haƙiƙa taɓaɓɓu sune waɗanda suka taɓar da kawu-kansu da iyalinsu ranar alkiya-ma". (sun taɓe da dauwamar da kansu a cikin wutada rashin saduwarsu izuwa matan aljanna waɗanda aka tanadar musu dasun bada gaskiya). Na'am wancanenka Shine ainihin taɓewa mabayyaniya.

15. Ruffai na wuta sun tabbata daga samansu akwai kuma ruffan wuta suna daga ƙasansu, wancanenka Allah yana ba wa ɓayinsa tsoro ne dashi (donsu tsorace shi), Yaku bayina kuji tsorona.

(ISHARA DA SAMA'A NA SUFAYE)

16. Waɗannan da suka nisanci gumaka da dukkan wanin Allah, wato suka nisanci bauta mata suka fuskanta izuwa Allah, albishir (da aljanna) ya tabbata a garesu, ka yiwa bayina albishir.

17. Waɗannan da suka sauraron magana su bi mafi kyansa, waɗancanenka sune waɗanda Allah ya shirye su,waɗancanenka sune ma'abota hankula.

18. Shin yanzu wanda kalmar azabata tabbata a gareshi (LA'AM LA'ANNA JAHANNAMA, har ya zuwa ƙarshen aya) to shin kaine wanda zaka tsamo wanda yake cikin wuta, (A'a).

19. Amma waɗanda sukaji tsoron Ubangijinsu benaye sun tabbata a garesu, da benaye ababan gini (suke sama da ita wato bene kan bene), ƙoramu suna gudana ƙarƙashinta (ƙarkashin benayen) Allah ya alkawaranta wannan alkawartawa, Allah baya saɓa alkawarinsa.

(WANNAN ITACE DUNIYA)

20. Shin baka sani ba haƙiƙa Ubangiji ya saukar da ruwa daga sama ya shigar dashi cikin maɓulɓulan ƙasa? Sannan yafito da hatsi dashi mai sabawar launinsa, sannan ya £eKashe sai ka ganshi kodadUe bayan korantaka, sannan ya maidashi dan daƙakKe a cikin wancanenka ak-wai gargaɗi ga ma'abota hankula.

أَفَمَن شَرَحَ اللَّهُ صَدْرَهُۥ لِلْإِسْلَٰمِ فَهُوَ عَلَىٰ نُورٍ مِّن رَّبِّهِۦ
فَوَيْلٌ لِّلْقَٰسِيَةِ قُلُوبُهُم مِّن ذِكْرِ اللَّهِ أُوْلَٰٓئِكَ فِي ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿21﴾
اللَّهُ نَزَّلَ أَحْسَنَ الْحَدِيثِ كِتَٰبًا مُّتَشَٰبِهًا مَّثَانِيَ تَقْشَعِرُّ
مِنْهُ جُلُودُ الَّذِينَ يَخْشَوْنَ رَبَّهُمْ ثُمَّ تَلِينُ جُلُودُهُمْ وَقُلُوبُهُمْ
إِلَىٰ ذِكْرِ اللَّهِ ذَٰلِكَ هُدَى اللَّهِ يَهْدِي بِهِۦ مَن يَشَآءُ وَمَن يُضْلِلِ اللَّهُ
فَمَا لَهُۥ مِنْ هَادٍ ﴿22﴾ أَفَمَن يَتَّقِي بِوَجْهِهِۦ سُوٓءَ الْعَذَابِ يَوْمَ الْقِيَٰمَةِ
وَقِيلَ لِلظَّٰلِمِينَ ذُوقُواْ مَا كُنتُمْ تَكْسِبُونَ ﴿23﴾ كَذَّبَ الَّذِينَ
مِن قَبْلِهِمْ فَأَتَىٰهُمُ الْعَذَابُ مِنْ حَيْثُ لَا يَشْعُرُونَ ﴿24﴾ فَأَذَاقَهُمُ
اللَّهُ الْخِزْيَ فِي الْحَيَوٰةِ الدُّنْيَا وَلَعَذَابُ الْآخِرَةِ أَكْبَرُ لَوْ كَانُواْ
يَعْلَمُونَ ﴿25﴾ وَلَقَدْ ضَرَبْنَا لِلنَّاسِ فِي هَٰذَا الْقُرْءَانِ
مِن كُلِّ مَثَلٍ لَّعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿26﴾ قُرْءَانًا عَرَبِيًّا غَيْرَ ذِي عِوَجٍ
لَّعَلَّهُمْ يَتَّقُونَ ﴿27﴾ ضَرَبَ اللَّهُ مَثَلًا رَّجُلًا فِيهِ شُرَكَآءُ
مُتَشَٰكِسُونَ وَرَجُلًا سَلَمًا لِّرَجُلٍ هَلْ يَسْتَوِيَٰنِ مَثَلًا الْحَمْدُ لِلَّهِ
بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿28﴾ إِنَّكَ مَيِّتٌ وَإِنَّهُم مَّيِّتُونَ ﴿29﴾
ثُمَّ إِنَّكُمْ يَوْمَ الْقِيَٰمَةِ عِندَ رَبِّكُمْ تَخْتَصِمُونَ ﴿30﴾

(HASKE DA BUdIN KIRJI DA ALƘUR'ANI)

21. Shin to wanda Allah ya buɓe ƙirjinsa da Musulunci ya shiriya, to shi yana kan haske daga Ubangijinsa, zai zama kamar wanda aka yimƙe bisa zuciyarsa to azabata tabbata ga waɗanda zukatan su take ƙeƙashe ga buran ƙarbar alƙur'ani, waɗancanenka suna cikin ɓata mabayyani.

22. Allah ya sassaukar da mafi kyan zance littafi mai kama da juna, abin maimaitawa (Alkawari da narko da waninsu), zukatan waɗanda suke jin tsoron Ubangijinsu take makyarkyata, tana tattara saboda tsoransa, sannan kuma ta nutsu, sannan kuma fa-tunsu da zukatansu suna nutsuwa (suna bege) izuwa ambaton Allah. Wancanenka (littafi) shiriyar Allah ne, da yake shiriyar wanda yaga dama dashi, wanda Allah ya ɓatar dashi ba mai shiryarwa a gareshi.

23. Shin wanda yake kare mummunar azabar Allah da zatin jikinsa (wato a jefa shi a wuta abin ƙuƙuncewar hannayensa izuwa wuyansa, sai zama kamar wanda ya aminta daga wannan dashiga aljanna?) Ance ga kafiran Makka "Ku ɗanɗani sakamakon abinda kuka kasance kuna aikatawa".

24. Waɗandasuke gabansu sun ƙaryata manzanninsu (cikin zuwan azaba), sai azabatazo musu ta gurin da basu sani ba.

25. Sai Allah ya ɗanɗana musu kunyata (shafewa da kashewa da zilla da waninsu) a cikin rayuwar duniya, kuma lallai azabar lahira tafi girma dasun kasance sunsan (azabartada bazasu karyata manzanni ba).

(MISALCE-MISALCE A CIKIN ALƘUR,ANI.

26. Haƙiƙa a cikin wannan Alƙur'ani mun sanyakowane misali donsu wa'azantu.

27. Alƙur'ani Balarabe, ba ma'abocin rikici da saɓawa ba, donsu suji tsoron kafirci.

28. Ubangiji ya saɓa misali (da mushiriki da mai kaɗaita Allah), mutum wanda masu tarayya suke cikinsa, masu kaushin hali da mutum sumul na mutum ɗaya zasuyidaidai a misali? (Wato bawan jama'a da bawan mutum ɗaya, bazasuyidaidai ba, don saboda bawan jama'a yayin da kowane ɗaya daga iyayen gijinsa ya nemi hidima tasa a lokaci ɗaya, saiya ɗimauta a cikin wa zai gabatar da hidima tasa, wannan misali ne ga mushuriki, na biyu, misali ne ga mai ɗayanta Allah) Godiya ta tabbata ga Allah shi kaɗai, bari! yawaicinsu mutanen Makka basu san (abinda zasu koma gareshi na azaba ba, saboda haka sukayi shirka).

29. Haƙiƙa kai (ya Annabi Sallallahu alaika wa sallama) zaka mutu ne, haƙiƙa su kuma zasu mutu ne (saboda haka badariyar ganganko ga mutuwa. Ta sauka ne yayin da suka gajinkirin mutuwarsa Sallallahu alaihi wa sallama).

30. Sannan haƙiƙa ku (yaku waɗannan mutane cikin abinda yake tsakaninsu na zalince-zalince) zakuyi husuma ranar alƙiyama nan ga Ubangijinku (wato ayi sakayyaga wanda aka zalinta ga wanda yayi zalunci).

حزب

۞ فَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن كَذَبَ عَلَى ٱللَّهِ وَكَذَّبَ بِٱلصِّدْقِ
إِذْ جَآءَهُۥٓ ۚ أَلَيْسَ فِى جَهَنَّمَ مَثْوًى لِّلْكَٰفِرِينَ ﴿31﴾ وَٱلَّذِى
جَآءَ بِٱلصِّدْقِ وَصَدَّقَ بِهِۦٓ ۙ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُتَّقُونَ ﴿32﴾
لَهُم مَّا يَشَآءُونَ عِندَ رَبِّهِمْ ۚ ذَٰلِكَ جَزَآءُ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿33﴾
لِيُكَفِّرَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ أَسْوَأَ ٱلَّذِى عَمِلُوا۟ وَيَجْزِيَهُمْ أَجْرَهُم
بِأَحْسَنِ ٱلَّذِى كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿34﴾ أَلَيْسَ ٱللَّهُ بِكَافٍ
عَبْدَهُۥ ۖ وَيُخَوِّفُونَكَ بِٱلَّذِينَ مِن دُونِهِۦ ۚ وَمَن يُضْلِلِ
ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِنْ هَادٍ وَمَن يَهْدِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن
مُّضِلٍّ ۗ أَلَيْسَ ٱللَّهُ بِعَزِيزٍ ذِى ٱنتِقَامٍ ﴿35﴾ وَلَئِن سَأَلْتَهُم
مَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ ۚ
قُلْ أَفَرَءَيْتُم مَّا تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ إِنْ أَرَادَنِىَ ٱللَّهُ
بِضُرٍّ هَلْ هُنَّ كَٰشِفَٰتُ ضُرِّهِۦٓ أَوْ أَرَادَنِى بِرَحْمَةٍ هَلْ هُنَّ
مُمْسِكَٰتُ رَحْمَتِهِۦ ۚ قُلْ حَسْبِىَ ٱللَّهُ ۖ عَلَيْهِ يَتَوَكَّلُ ٱلْمُتَوَكِّلُونَ ﴿36﴾
قُلْ يَٰقَوْمِ ٱعْمَلُوا۟ عَلَىٰ مَكَانَتِكُمْ إِنِّى عَٰمِلٌ ۖ فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ
مَن يَأْتِيهِ عَذَابٌ يُخْزِيهِ وَيَحِلُّ عَلَيْهِ عَذَابٌ مُّقِيمٌ ﴿37﴾

(WANENE YA FI KOWA ZALINCI-WANENE YAFI SU GASKIYA)

31. Waye mafi zalinci bisa Ubangiji fiyeda wanda yayi ƙarya (da dangana shriki izuwa Ubangiji?) Ya ƙaryata gaskiya (Shine Alƙur'ani) zamanin dayazo masa (ba mafi ƙarya daga gareshi). Shin makomar kafirai ba a cikin jahannama bane? (Cikin jahannama take).
32. Wanda yazoda gaskiya (Shine Annabi Sallallahu alaihi wa sallama) da waɗanda suka gaskatashi (sune masu jin tsoron Allah (marassa shirka).
33. Abinda suke bukata wajen Ubangijinsu yana garesu, wan-canenka Shine sakamakon masu kyakkyawan aiki (saboda ima-ninsu).
34. Allah ya yassare musu wannan domin ya kankare musu mummunan abinda suka aikata, ya saka musa ladansu da kyakykyawan abinda suka kasance suna aikatawa.
35. Shin Ubangiji ba ma'ishin bawansa bane? Suna baka tsoro da waɗanda suke wanin Allah, (sune gumaka, su kashe shi, ko kuma su ɓata hankalinsa), duk wanda Allah ya ɓatar dashi to babu mai shiryarwa gareshi, wanda Allah ya shirye shi to ba mai ɓatarwa gareshi. Shin Ubangiji ba mai rinjaye bane bisa al'amarinsa, mai azabadaga magautansa? (BALA) mai rinjaye ne).

(MUNAKASHAR MUSHURIKAI A CIKIN BAUTARSU GAGUMAKA)

36. Wallahi inka tambaye su waye halicci sammai da ƙassa? Lallai zasu ce dakai "Allah ne", Cene, "Ku bani labarin abinda kuke bautawa ba Allah ba (na gumaka), in Ubangiji ya nufe ni da tsanani yalla su masu yayewa ne ga tsananin nasa? (A'a), ko in ya nufe ni da rahama yalla ko su zasu riƙe rahamar tasane! Cene, "Allah ne ma'ishina, masu dogaro su dogara a kansa"
37. Cene, "Yaku mutanena kuyi aiki bisa halinku, haƙiƙa ni mai aiki ne bisa halina, to da sannu zaku san wanda azabaza tazo masa ta kunyatar dashi, kuma azaba madauwamiya zata sauka gareshi. Haƙiƙa (Allah yakunyatar dasu a Badar).

إِنَّآ أَنزَلْنَا عَلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ لِلنَّاسِ بِٱلْحَقِّ فَمَنِ ٱهْتَدَىٰ
فَلِنَفْسِهِۦ وَمَن ضَلَّ فَإِنَّمَا يَضِلُّ عَلَيْهَا وَمَآ أَنتَ عَلَيْهِم
بِوَكِيلٍ ﴿38﴾ ٱللَّهُ يَتَوَفَّى ٱلْأَنفُسَ حِينَ مَوْتِهَا وَٱلَّتِي لَمْ تَمُتْ
فِي مَنَامِهَا فَيُمْسِكُ ٱلَّتِي قَضَىٰ عَلَيْهَا ٱلْمَوْتَ وَيُرْسِلُ ٱلْأُخْرَىٰ
إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَتَفَكَّرُونَ ﴿39﴾
* أَمِ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ شُفَعَآءَ قُلْ أَوَلَوْ كَانُواْ لَا يَمْلِكُونَ شَيْـًٔا ثمن
وَلَا يَعْقِلُونَ ﴿40﴾ قُل لِّلَّهِ ٱلشَّفَٰعَةُ جَمِيعًا لَّهُۥ مُلْكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ثُمَّ إِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿41﴾
وَإِذَا ذُكِرَ ٱللَّهُ وَحْدَهُ ٱشْمَأَزَّتْ قُلُوبُ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ
بِٱلْءَاخِرَةِ وَإِذَا ذُكِرَ ٱلَّذِينَ مِن دُونِهِۦٓ إِذَا هُمْ يَسْتَبْشِرُونَ ﴿42﴾
قُلِ ٱللَّهُمَّ فَاطِرَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ عَٰلِمَ ٱلْغَيْبِ
وَٱلشَّهَٰدَةِ أَنتَ تَحْكُمُ بَيْنَ عِبَادِكَ فِي مَا كَانُواْ
فِيهِ يَخْتَلِفُونَ ﴿43﴾ وَلَوْ أَنَّ لِلَّذِينَ ظَلَمُواْ مَا فِي ٱلْأَرْضِ
جَمِيعًا وَمِثْلَهُۥ مَعَهُۥ لَافْتَدَوْاْ بِهِۦ مِن سُوٓءِ ٱلْعَذَابِ يَوْمَ
ٱلْقِيَٰمَةِ وَبَدَا لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ مَا لَمْ يَكُونُواْ يَحْتَسِبُونَ ﴿44﴾

(TABBATAR DA WAHADANIYAR ALLAH DA IKONSA TAREDA MUNAƘASHARSU DA BAYANIN SAKAMAKONSU)

38. Haƙiƙa mun saukar da littafi a gareka da gaskiya don (shiryar da) mutane, to wanda ya shiriya, ya shinya don kansa, wanda ya ɓata, to dahir dai ya ɓata a kan kansa. Kai ba wakili ne a kansu ba (bare ka tilashe su kan shiriya).

39. Ubangiji yana karɓe rayuka yayin mutuwarta, yana karɓar wacce bata mutu ba a cikin baccinta, ya rƘe wacce ya hukunta mutuwa a kanta ya saki ɗayar izuwa ajali abin ambato, (wato wacce ake sakin Itacc rai mai rarrabcwa da al'amura, haƙiƙanin rayuwa tana wanzuwa ba tareda ita ba, saɓanin sunkuye). Haƙiƙa akwai ayoyi a cikin wancanenka (abin ambato) ga mutane masuyin tunani. Su sani cewa mai iko bisa wancanenka mai ikone bisa tashin alƙiyama, Kuraishu Kuwa basuyitunani a cikin wannan ba).

40. Shin sun riƙi gumaka masu ceto ne (nan ga Allah ba Allah ba?)Cene (dasu) "yanzu kuwa zasuyiceto kodasun kasance basu mallaki komai ba (na ceton da waninta) basu hankaƙi komai (na ceton) ba, (wala wanin wannan. La, bazasu iyaceto ba).

41. Cene, "Ceto ga Allah yake baki daya (saboda haka ba wandazaiyi ceto saida izinin Allah), Mulkin sammai da ƙassaina ga Ubangiji, sannan izuwa Ubangiji ake komawa da ku.

42. Idan aka ambaci Allah shi kaɗai (ba tareda gumakansu ba), zukatan wanda basu bada gaskiya da Ubangiji ba takan yankwane, in an ambaci waɗanda suke bashi ba, sai gasu suna farin ciki.

43. Cene, "Ya Ubangiji mai ƙagen sammai da ƙassai masanin asirin fake dana sarari, kaine kake hukunci tsakanin bayinka a cikin abinda suka kasance suna sassaɓawa a cikinsa (na daga gaskiya).

44. Da haƙiƙa abinda yake cikin ƙasa baki ɗaya da misalinsa tare dashi yana ga waɗanda sukayi zalinci, da sai sun yi fansa dashi daga mummunar azaba ranar alƙiyama, abinda basu kasance sun zace shi baya bayyana garesu.

وَبَدَا لَهُمْ سَيِّـَٔاتُ مَا كَسَبُواْ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿٤٥﴾
فَإِذَا مَسَّ ٱلْإِنسَانَ ضُرٌّ دَعَانَا ثُمَّ إِذَا خَوَّلْنَٰهُ نِعْمَةً مِّنَّا
قَالَ إِنَّمَا أُوتِيتُهُۥ عَلَىٰ عِلْمٍ بَلْ هِىَ فِتْنَةٌ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ
لَا يَعْلَمُونَ ﴿٤٦﴾ قَدْ قَالَهَا ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ فَمَا أَغْنَىٰ عَنْهُم
مَّا كَانُواْ يَكْسِبُونَ ﴿٤٧﴾ فَأَصَابَهُمْ سَيِّـَٔاتُ مَا كَسَبُواْ وَٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ
مِنْ هَٰٓؤُلَآءِ سَيُصِيبُهُمْ سَيِّـَٔاتُ مَا كَسَبُواْ وَمَا هُم بِمُعْجِزِينَ ﴿٤٨﴾
أَوَلَمْ يَعْلَمُواْ أَنَّ ٱللَّهَ يَبْسُطُ ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقْدِرُ
إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَأَيَٰتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿٤٩﴾ ۞ قُلْ يَٰعِبَادِىَ ٱلَّذِينَ
أَسْرَفُواْ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ لَا تَقْنَطُواْ مِن رَّحْمَةِ ٱللَّهِ إِنَّ ٱللَّهَ
يَغْفِرُ ٱلذُّنُوبَ جَمِيعًا إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٥٠﴾ وَأَنِيبُواْ
إِلَىٰ رَبِّكُمْ وَأَسْلِمُواْ لَهُۥ مِن قَبْلِ أَن يَأْتِيَكُمُ
ٱلْعَذَابُ ثُمَّ لَا تُنصَرُونَ ﴿٥١﴾ وَٱتَّبِعُوٓاْ أَحْسَنَ مَآ أُنزِلَ إِلَيْكُم
مِّن رَّبِّكُم مِّن قَبْلِ أَن يَأْتِيَكُمُ ٱلْعَذَابُ بَغْتَةً
وَأَنتُمْ لَا تَشْعُرُونَ ﴿٥٢﴾ أَن تَقُولَ نَفْسٌ يَٰحَسْرَتَىٰ عَلَىٰ
مَا فَرَّطتُ فِى جَنۢبِ ٱللَّهِ وَإِن كُنتُ لَمِنَ ٱلسَّٰخِرِينَ ﴿٥٣﴾

ربع

45. Sakamakon miyagun abinda suka aikata ya bayyana garesu, (abinda suke izgili dashiya sauka a kansu Shine azaba).

(HAKA MUTUM YAKE)

46. Idan tsanani ya sami mutum saiya kira mu, ya rinƙa roƙon mu, sannan idan muka sanya masa ni'ima daga garemu sai yace "Dahir dai an bani wannan a bisa ilimi (daga Allah cewa ni na cancanci wannan ni'ima tawa). Bari! ita wannan magana jarraba ce daga Allah (yake jarrabar bawa da ita) saidai ya-wancinsu basu san (cewwa baiwan nan maƙarƙashiyace ba).

47. Haƙiƙa waɗanda suke gabansu (na ɗaga al'umma) sun faɗi wannan magana (kamar Kamna da makamancinsa) abinda suke tsomrta ba wadatar musu da ko-mai ba.

48. Sai sakamakon miyagun abinda suka aikata ya same su, waɗanda sukayi zalinci daga waɗannan (Kuraishawa) da sannu sakamakon miyagun abinda suka aikata zai same su, su bazasu tserewa azabar Ubangiji ba, (sai akayi masu fari, sannan aka yalwata a garesu).

49. Shin basu sani bane cewa Ubangiji Allah Shine yake shinfida arziki ga wanda yaga dama bane? Yana ƙuntatawa ga wan-dayaga dama (don jarrabawa ga kowanne, wanda aka yalwata masa to an yi ne don a gani ko ya daure. Allah yana yalwata arziki ga wanda yaga dama ne komai da'a komai ma'asiya, yana ƙuntatawar arziki ga wanda yaga dama ne komai da'a komai ma'asiya, hikimar wannan jarrabawar ga kowane daga cikinsu Shine don a gani zai daure ko bazai daure ba, zai gode ko bazai gode ba), haƙiƙa akwai ayoyi cikin wancanenka ga mutane da suka bada gaskiya da Ubangiji.

(YALWAR RAHAMAR ALLAH TAREDA WA'AZI DASHIRYARWA)

50. Cene, "Yaku bayina waɗanda sukayi ɓarna bisa kawukansu kadaku ,ɗebe haso daga rahamar Allah, haƙiƙa Allah yana gafarta zunubai baki dayansu (ga wanda ya tubadaga shirka) haƙiƙa shi Ubangiji Shine mai gafara mai yawan jinƙai.

51. Ku koma izuwa Ubangijinku, ku tsarkake aiki donsa, tun gaban azaba batazo muku ba, sannan baza a taimake ku ba (da hana azaban nan inbaku tuba ba).

52. Kubi kyakykyawan abinda aka saukar izuwa gareku daga Ubangijinku, (Shine alƙur'ani) tun gaban azaba batazo muku ba, barabe alhali ku bakuyi hasashe ga zuwan ta ba.

53. Tun gaban kai ba tace, "Ya tabewata! (wato ya nadamata!) bisa sakacin da nayi a janibin Allah, haƙiƙa ni na kasance cikin masu wasa (da addininsu da littafinsa!)

أَوْ تَقُولَ لَوْ أَنَّ اللَّهَ هَدَىٰنِي لَكُنتُ مِنَ الْمُتَّقِينَ ﴿54﴾ أَوْ تَقُولَ
حِينَ تَرَى الْعَذَابَ لَوْ أَنَّ لِي كَرَّةً فَأَكُونَ مِنَ الْمُحْسِنِينَ ﴿55﴾
بَلَىٰ قَدْ جَآءَتْكَ ءَايَٰتِي فَكَذَّبْتَ بِهَا وَاسْتَكْبَرْتَ وَكُنتَ
مِنَ الْكَٰفِرِينَ ﴿56﴾ وَيَوْمَ الْقِيَٰمَةِ تَرَى الَّذِينَ كَذَبُوا عَلَى اللَّهِ
وُجُوهُهُم مُّسْوَدَّةٌ أَلَيْسَ فِي جَهَنَّمَ مَثْوًى لِّلْمُتَكَبِّرِينَ ﴿57﴾
وَيُنَجِّي اللَّهُ الَّذِينَ اتَّقَوْا بِمَفَازَتِهِمْ لَا يَمَسُّهُمُ السُّوٓءُ وَلَا هُمْ
يَحْزَنُونَ ﴿58﴾ اللَّهُ خَالِقُ كُلِّ شَيْءٍ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ وَكِيلٌ ﴿59﴾
لَّهُ مَقَالِيدُ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَالَّذِينَ كَفَرُوا بِـَٔايَٰتِ اللَّهِ
أُولَٰٓئِكَ هُمُ الْخَٰسِرُونَ ﴿60﴾ قُلْ أَفَغَيْرَ اللَّهِ تَأْمُرُونِي
أَعْبُدُ أَيُّهَا الْجَٰهِلُونَ ﴿61﴾ وَلَقَدُ اُوحِيَ إِلَيْكَ
وَإِلَى الَّذِينَ مِن قَبْلِكَ لَئِنْ أَشْرَكْتَ
لَيَحْبَطَنَّ عَمَلُكَ وَلَتَكُونَنَّ مِنَ الْخَٰسِرِينَ ﴿62﴾ بَلِ اللَّهَ
فَاعْبُدْ وَكُن مِّنَ الشَّٰكِرِينَ ﴿63﴾ * وَمَا قَدَرُوا اللَّهَ ثمن
حَقَّ قَدْرِهِۦ وَالْأَرْضُ جَمِيعًا قَبْضَتُهُۥ يَوْمَ الْقِيَٰمَةِ وَالسَّمَٰوَٰتُ
مَطْوِيَّٰتُۢ بِيَمِينِهِۦ سُبْحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿64﴾

54. Ko tace, "da Allah ya shirye ni (da da'a) dana kasance daga cikin masu tsoron Allah".
55. Ko tace, zamanin data ga azaba, "dayakace ina da komowa izuwa duniya in kasance daga masu kyakykyawan aiki".
56. Sai a ce (dashi daga Ubangiji) "I ayoyina sun zo maka (Shine alƙur'ani, shi ko sababin shiriya ne), ka ƙaryatada ita, kayi gir-man kai ga buran imani da ita, ka kasance cikin kafirai.

(MAKOMAR MATUKABBIRAI DA KIRARI GA ALLAH)

57. A ranar alƙiyama kana ganin waɗanda sukayi ƙarya bisa Ubangiji (da dangana ɗa izuwa gareshi), fuskokinsu baƙiƙƙirin, shin makomar masu girman kai ga buran imani bata kasance ta wutar jahannama bane? (BALA! ta kasance).
58. Ubangiji yana tserar da waɗanda sukaji tsoronsa daga jahannama a gurin tsiransu na Aljanna, (Shine a sanya su a gurin tsiran, mummunan abu bazai shafe su ba, su bazasuyibaƙin ciki ba).
59. Allah ne mahaliccin kowane abu, shi mai ikone bisa komai, (yana sarrafawa yadda yaga dama).
60. Mabudan taskokin sammai da ƙassai (na ruwa da tsiri da waninsu) yana ga Allah, waɗanda suka kafirtada ayoyin Allah (sune Alƙur'ani), wadancanenka sune taɓaɓɓu.
61. Kace "yanzu shin wanin Allah kuke umarnina in bautawa yaku waɗannan jahilai?".
62. Haƙika an aiko izuwa gareka da waɗannan dasuke gabanka, Wallahi lallai in kayi shirka (Ya Muhammadu Sallallahu alaika wa sallama a ƙaddare), Lallai aikinka zai lalace, lallai zaka kasance daga taɓaɓɓu.
63. Bari! Allah kaɗai zaka bautawa, ka kasance daga masu godewa ni'imominsa.
64 Basu girmama Allah haƙiƙar girmama shi ba, ƙassai dukkansu mulkin Allah ne, (ma'ana dukkansu ƙasa gaba ɗayanta a cikin danƙin Allah take) ranar alƙiyama, sammai ababan tattarawa ne a cikin ikon Allah, tsar-ki ya tabbatar masa ya girmama ga buran abinda suke shirkantawa dashi.

وَنُفِخَ فِي اِ۬لصُّورِ فَصَعِقَ مَن فِي اِ۬لسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِي اِ۬لْأَرْضِ
إِلَّا مَن شَآءَ اَ۬للَّهُ ثُمَّ نُفِخَ فِيهِ أُخْرَىٰ فَإِذَا هُمْ قِيَامٌ
يَنظُرُونَ ﴿65﴾ وَأَشْرَقَتِ اِ۬لْأَرْضُ بِنُورِ رَبِّهَا وَوُضِعَ
اَ۬لْكِتَٰبُ وَجِيٓءَ بِالنَّبِيٓـِٔينَ وَالشُّهَدَآءِ وَقُضِيَ بَيْنَهُم بِالْحَقِّ
وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿66﴾ وَوُفِّيَتْ كُلُّ نَفْسٍ مَّا عَمِلَتْ
وَهُوَ أَعْلَمُ بِمَا يَفْعَلُونَ ﴿67﴾ وَسِيقَ اَ۬لَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِلَىٰ جَهَنَّمَ
زُمَرًا حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُوهَا فُتِّحَتْ أَبْوَٰبُهَا وَقَالَ لَهُمْ خَزَنَتُهَآ
أَلَمْ يَأْتِكُمْ رُسُلٌ مِّنكُمْ يَتْلُونَ عَلَيْكُمْ ءَايَٰتِ رَبِّكُمْ وَيُنذِرُونَكُمْ
لِقَآءَ يَوْمِكُمْ هَٰذَا قَالُواْ بَلَىٰ وَلَٰكِنْ حَقَّتْ كَلِمَةُ اُ۬لْعَذَابِ
عَلَى اَ۬لْكَٰفِرِينَ ﴿68﴾ قِيلَ اَ۟دْخُلُوٓاْ أَبْوَٰبَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَا فَبِئْسَ
مَثْوَى اَ۬لْمُتَكَبِّرِينَ ﴿69﴾ وَسِيقَ اَ۬لَّذِينَ اَ۪تَّقَوْاْ رَبَّهُمْ إِلَى اَ۬لْجَنَّةِ
زُمَرًا حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُوهَا وَفُتِّحَتْ أَبْوَٰبُهَا وَقَالَ لَهُمْ خَزَنَتُهَا
سَلَٰمٌ عَلَيْكُمْ طِبْتُمْ فَادْخُلُوهَا خَٰلِدِينَ ﴿70﴾ وَقَالُواْ
اُ۬لْحَمْدُ لِلَّهِ اِ۬لَّذِي صَدَقَنَا وَعْدَهُۥ وَأَوْرَثَنَا اَ۬لْأَرْضَ
نَتَبَوَّأُ مِنَ اَ۬لْجَنَّةِ حَيْثُ نَشَآءُ فَنِعْمَ أَجْرُ اُ۬لْعَٰمِلِينَ ﴿71﴾

65. An yi busa a cikin Kaho, (busa ta biyu), wanda yake sammai da wanda yake ƙassaiya mutu sai wanda Allah yaga dama (na daga 'yammatan Aljanna da samarin aljanna da waninsu), sannan aka sake busa a wata marrar sai gasu a tsaye suna duban abindaza a aika dasu.
66. Ƙasa tayi haske da hasken Ubangijinta (zamanin daya bayyana saboda rabe hukunci) aka ajiye littafin (ayyuka saboda hisabi) aka zoda Annbawa da Shahidai (wato al'ummatasa da zasu zo) ga ma'aika cewa sun isar da aike) akayi hukunci tsakaninsu da adaƙi, su baza a zalince su komai ba.
67. Aka cikawa kowace kai sakamakon abindata aikata, Allah ne masani da abinda suke aikatawa, (Shine masani da abinda suka aikata, baya bukata izuwa mai shaida).
68. An kora waɗanda suka kafirtada tsanani izuwa jahannama bundu-bundu har yayin da sukazo mata aka buɗe ƙofofinta ma-taskatanta suke ce dasu, "Shin manzanni daga gareku ba, su zo muku bane suna karantarwar ayoyin Ubangiji a gareku? (Shine alƙur'ani da waninsa), suna tsoratar dasu da saduwarku (Shine ranar ku wannan"). Sukace, "BALA!. sun zo mana, saidai kalmar azaba ce ta tabbata bisa kafirai (wato Itace LA AM LA ANNA JAHANNAMA).
69. Aka ce, "Ku shiga ƙofofin jahannama masu dauwama a cikinta, tir! Makoma ta masu girman kaijahannamu".
70. Aka kora waɗanda suke tsoron Ubangijinsu da luɗfi izuwa Aljanna bundu-bundu (wato jama'a-jama'a) har yayin da sukazo mata alhali haƙiƙa da ma an buɗe ƙofofinta masu tsaronta sukace dasu "SALAMUN ALAIKUM, kun ji daɗi. To ku shigeta kuna masu dauwama (ababan ƙaddarawan dauwama a cikinta, to sai suka shigeta. Akace kora su da buɗe ƙofofi tun gaban basu zo ba ban girma ne garesu. Korawar kafirai da buɗe ƙofifin Jahanna yayin zuwan su, don zafinta ya sadu izuwa garesu wulaƙantarwa ne.
71. (Suke shigeta) sukace, "Godiya ta tabbata ga Ubangiji wanda ya cika mana alkawarinsa (Shine aljanna) yagada mana ƙasar Aljanna muna zama a cikin aljanna inda duk muka ga dama, (domin cewa ita dukkan ta ba inda zakace nan yafi nan kyau). Madalla ladan masu aiki (aljanna).

وَتَرَى الْمَلَٰٓئِكَةَ حَآفِّينَ مِنْ حَوْلِ الْعَرْشِ يُسَبِّحُونَ بِحَمْدِ
رَبِّهِمْ وَقُضِيَ بَيْنَهُم بِالْحَقِّ وَقِيلَ الْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ الْعَٰلَمِينَ ﴿72﴾

40 سُورَةُ غَافِرٍ مَكِّيَّةٌ
وَهِيَ أَرْبَعٌ وَثَمَانُونَ ءَايَةً 84

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

* حمٓ ﴿1﴾ تَنزِيلُ الْكِتَٰبِ مِنَ اللَّهِ الْعَزِيزِ الْعَلِيمِ ﴿2﴾ غَافِرِ الذَّنبِ وَقَابِلِ
التَّوْبِ شَدِيدِ الْعِقَابِ ذِي الطَّوْلِ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ إِلَيْهِ الْمَصِيرُ ﴿2﴾
مَا يُجَٰدِلُ فِيٓ ءَايَٰتِ اللَّهِ إِلَّا الَّذِينَ كَفَرُواْ فَلَا يَغْرُرْكَ تَقَلُّبُهُمْ
فِي الْبِلَٰدِ ﴿3﴾ كَذَّبَتْ قَبْلَهُمْ قَوْمُ نُوحٍ وَالْأَحْزَابُ مِنۢ بَعْدِهِمْ
وَهَمَّتْ كُلُّ أُمَّةٍ بِرَسُولِهِمْ لِيَأْخُذُوهُ وَجَٰدَلُواْ بِالْبَٰطِلِ لِيُدْحِضُواْ
بِهِ الْحَقَّ فَأَخَذْتُهُمْ فَكَيْفَ كَانَ عِقَابِ ﴿4﴾ وَكَذَٰلِكَ حَقَّتْ كَلِمَتُ
رَبِّكَ عَلَى الَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَنَّهُمْ أَصْحَٰبُ النَّارِ ﴿5﴾ الَّذِينَ يَحْمِلُونَ
الْعَرْشَ وَمَنْ حَوْلَهُ يُسَبِّحُونَ بِحَمْدِ رَبِّهِمْ وَيُؤْمِنُونَ بِهِ
وَيَسْتَغْفِرُونَ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ رَبَّنَا وَسِعْتَ كُلَّ شَيْءٍ رَّحْمَةً وَعِلْمًا
فَاغْفِرْ لِلَّذِينَ تَابُواْ وَاتَّبَعُواْ سَبِيلَكَ وَقِهِمْ عَذَابَ الْجَحِيمِ ﴿6﴾

ربع

72. Kana kallon Mala'iku (Ya Annabi Sallallahu alaihi wa sallama) suna masu kewayewa daura da Al'arshi (sun yi sahu-sahu daga kowace nahiya) suna yin tasbihi da godiyar Ubangijinsu (wato suna cewa SUBHANALLA-HI WA BIHAMDIHI). An yi hukunci tsakanin talikai da goskiya (sai a shigar da miminai aljanna, kafirai kuma wuta), akace (dasu) godiya ta tabbata ga Ubangiji Ubangijin talikai (Ya cika tabbatar wađannan jama'ar guda biyu da godiyar Mala'ikuda sauran 'yan aljanna don saboda Ubangiji ya basu rabo mai girma).

Wannan Saratul Mumini ce

A Makka aka saukar da ita Aya Tamanin da Hudu ce (84)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba đaya, mai jinƙan Muminai a lahira akeɓe

(Ita Wannan Sura An Fara Ne Da HA-Mi-M, Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wa Sallama Yana Yiwa Wađannan Surori Masu Farawa Da HA-MIM-Kirari Da Amaren Alƙur'ani Da Kuma Munaƙasha Da Masu Jayayya Ranar alƙiyama Da Tabbatar Tashin alƙiyama Da Tabbatar Da Risala Da Halin Mushurkai Da Masu Jayayya Ranar alƙiyama Da ƙissar Fir'auna Da Hamana Da Karuna Don saɓa Misali Ga Mushurkai Da Kwatanta Allah Da Dukkan Kamala Da Tsarkake Shi Ga Buran Dukkan Tawaya).

1. Allahu a'alamu bi muradihi bi zalika, saukarwar Alƙur'ani daga Allah ne Mabuwayi (cikin mulkinsa), masani (da halittarsa).
2. Mai gafarta zunuban (Muminai), mai karɓar tubansu, mai tsananin ukuba (ga kafirai). mai ni'imtawa tutur (mai gafara tutur hakana mai karɓar tuba) ba abin bautawa da gaskiya sai Allah, makoma ya tabbata izuwa gareshi.
3. Ba mai jayayya cikin alƙur'ani sai wađanda suka kafirta (daga mutanen Makka), kada wandakarsu a garuruwa ta ruđe ka. Haƙiƙa karhhensu wuta).
4. Mutanen Annabi Nuhu sun ƙaryata (manzanninsu) da runduna (kamar Adu Samudu da waninsu) daga bayansu kowane mutanen al'umma tayi nufi da manzon su su kama shi (donsu kashe shi), sun yi jayayya ta ƙarya donsu rushe, gaskiya dashi wannan ƙaryar, saina kama su da azabata. To yaya uƙubata ta kasance? (Ta akfu gurin afkuwarta).
5. Hakana kalmar Ubangijinka ta tabbata (LA AM LA ANNA JA-HANNAMA) a bisa wađanda suka kafirta, haƙiƙa sune 'yan wuta.
6. Wađanda suke đauke da Al'arshi da Mala'iku kambawa dasuke daura dashi suna yin tasbihi tareda godiyar Ubangijinsu suna cewa "SUBHANALLAHI WA BI HAMDIHI) suna bada gaskiya dashi (da zukatansu) suna neman gafara ga wađanda suka bada gaskiya suna cewa "Ya Ubangijinmu rahamarka da iliminka sun yalwaci komai, kayi gafara ga wađanda suka tuba (daga shirka) sukabi hanyar ka (Shine addinin Musulunci) ka kiyashe su azabar wuta.

رَبَّنَا وَأَدْخِلْهُمْ جَنَّٰتِ عَدْنٍ اِ۬لَّتِے وَعَدتَّهُمْ وَمَن صَلَحَ
مِنْ ءَابَآئِهِمْ وَأَزْوَٰجِهِمْ وَذُرِّيَّٰتِهِمُۥٓ إِنَّكَ أَنتَ اَ۬لْعَزِيزُ
اُ۬لْحَكِيمُ ﴿7﴾ وَقِهِمُ اُ۬لسَّيِّـَٔاتِ وَمَن تَقِ اِ۬لسَّيِّـَٔاتِ يَوْمَئِذٖ
فَقَدْ رَحِمْتَهُۥ وَذَٰلِكَ هُوَ اَ۬لْفَوْزُ اُ۬لْعَظِيمُ ﴿8﴾ * إِنَّ اَ۬لَّذِينَ ثمن
كَفَرُواْ يُنَادَوْنَ لَمَقْتُ اُ۬للَّهِ أَكْبَرُ مِن مَّقْتِكُمُۥٓ أَنفُسَكُمُۥٓ
إِذْ تُدْعَوْنَ إِلَى اَ۬لْإِيمَٰنِ فَتَكْفُرُونَ ﴿9﴾ قَالُواْ
رَبَّنَا أَمَتَّنَا اَ۪ثْنَتَيْنِ وَأَحْيَيْتَنَا اَ۪ثْنَتَيْنِ فَاعْتَرَفْنَا بِذُنُوبِنَا
فَهَلْ إِلَىٰ خُرُوجٖ مِّن سَبِيلٖ ﴿10﴾ ذَٰلِكُم بِأَنَّهُۥٓ إِذَا دُعِيَ
اَ۬للَّهُ وَحْدَهُۥ كَفَرْتُمْ وَإِن يُشْرَكْ بِهِۦ تُؤْمِنُواْ فَالْحُكْمُ لِلَّهِ
اِ۬لْعَلِيِّ اِ۬لْكَبِيرِ ﴿11﴾ هُوَ اَ۬لَّذِے يُرِيكُمُۥٓ ءَايَٰتِهِۦ وَيُنَزِّلُ
لَكُم مِّنَ اَ۬لسَّمَآءِ رِزْقاٗ وَمَا يَتَذَكَّرُ إِلَّا مَنْ يُّنِيبُ ﴿12﴾ فَادْعُواْ اُ۬للَّهَ
مُخْلِصِينَ لَهُ اُ۬لدِّينَ وَلَوْ كَرِهَ اَ۬لْكَٰفِرُونَ ﴿13﴾ رَفِيعُ اُ۬لدَّرَجَٰتِ
ذُو اُ۬لْعَرْشِ يُلْقِے اِ۬لرُّوحَ مِنْ أَمْرِهِۦ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ
لِيُنذِرَ يَوْمَ اَ۬لتَّلَاقِ ﴿14﴾ يَوْمَ هُم بَٰرِزُونَ لَا يَخْفَىٰ عَلَى اَ۬للَّهِ
مِنْهُمْ شَےْءٞ لِّمَنِ اِ۬لْمُلْكُ اُ۬لْيَوْمَ لِلَّهِ اِ۬لْوَٰحِدِ اِ۬لْقَهَّارِ ﴿15﴾

7. "Ya Ubangijinmu ka shigar dasu aljannar dauwama wacce kayi musu alkawari da itada waɗanda suka gyattu na daga iyayensu da matayensu da zurriyoyinsu, haƙiƙa kaine mabuwayi gwani.
8. Ka kiyashe su azabar miyagun ayyuka, wandaka kiyashe shi azabar miyagun ayyuka ranar alƙiyama, to haƙiƙa ka jiƙansa, wancanenka Shine rabo mai gir-ma.

WANI ABU DAGA TSARMAKATAN RANAR ALƘIYAMA)

9. Haƙiƙa waɗanda suka kafirta ana kiransu (daga katarnin Mala'iku alhali suna zargin kansu yayin shiga wutar) "Lallai ƙin da Allah yake musu da zargin Shine yafi girma daga zargin da kuke wa kawukanku zamanin da ake kiranku izuwa imani a duniyakuna kafircewa".
10. Sai sukace "Ya Ubangijinmu ka karƙi ranmu sau biyu ka raya mu sau biyu, (saboda su suna ɗigon ƙazanta matattu ne aka raya su, sannan aka karɓi ransu, sannan aka raya su saboda tashin alƙiyama) To mukayi furuci da zunubanmu (wato kafircinmu da ƙaryatawarmu da Alƙiyama) yalla akwai dama izuwa fita (daga wuta, da komawa izuwa duniya domin mu bi ka, jawabi babu).
11. Wancanenku azaba (da kuke cikinsa), saboda cewa haƙiƙa a idan an kira Allah (a duniya) shi ka-dai, sai ku kafirta (da kadaitashi), in an yi shirka dashi sai ku bada gaskiya (dashirkar), to hukunci (a cikin yi muku azaba) ya tabbata ga Ubangiji madau-kaki, mai girma.
12. Shine wanda yake nuna muku ayoyin wahadaniyyarsa (wato kadTaitarsa) yake saukar mukuda arzikinsa daga sama (Shine ruwa), ba mai wa'azantuwa sai wanda yakoma izuwa Allah, (yabar shirka).
13. To ku bautawa Allah kuna masu tsarkakae bauta a gareshi, koda kafiran sun ki (tsarkakewarku daga shirka).
14. Ubangiji madaukakin darajoji ne, (ai mai daukaka darajoji ne cikin aljanna) mahaliccin al'arshi yana saukar da wahayi (na daga maganarsa) ga wanda yaga dama na daga bayinsa do-min ya tsoratar da mutane ranar alƙiyama (wato ranar gamuwar mazowa sama da ƙasa da mai bautada abin bautawa da mai zalinci da abin zalinta a cikin-sa).
15. Ranar da zasu fito daga cikin kaburburansu babu abinda yake ɓuyaga ubangiji daga garesu, mulki ga wa yake a yau? (Ubangiji ne mai fadawa kansa Shine mai amsawa kansa, yace) "Yana ga Allah maɗayancin Sarki mai rinjaye (ga halittarsa).

ٱلْيَوْمَ تُجْزَىٰ كُلُّ نَفْسٍۭ بِمَا كَسَبَتْ ۚ لَا ظُلْمَ ٱلْيَوْمَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ
سَرِيعُ ٱلْحِسَابِ ﴿17﴾ وَأَنذِرْهُمْ يَوْمَ ٱلْـَٔازِفَةِ إِذِ ٱلْقُلُوبُ
لَدَى ٱلْحَنَاجِرِ كَـٰظِمِينَ ۚ ﴿18﴾ مَا لِلظَّـٰلِمِينَ مِنْ حَمِيمٍ وَلَا شَفِيعٍ
يُطَاعُ ﴿19﴾ يَعْلَمُ خَآئِنَةَ ٱلْأَعْيُنِ وَمَا تُخْفِى ٱلصُّدُورُ ﴿20﴾ وَٱللَّهُ يَقْضِى
بِٱلْحَقِّ ۖ وَٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِهِۦ لَا يَقْضُونَ بِشَىْءٍ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ
هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْبَصِيرُ ﴿21﴾ * أَوَلَمْ يَسِيرُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ فَيَنظُرُوا۟
كَيْفَ كَانَ عَـٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ كَانُوا۟ مِن قَبْلِهِمْ ۚ كَانُوا۟ هُمْ
أَشَدَّ مِنْهُمْ قُوَّةً وَءَاثَارًا فِى ٱلْأَرْضِ فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُ بِذُنُوبِهِمْ
وَمَا كَانَ لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ مِن وَاقٍ ﴿22﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ
كَانَت تَّأْتِيهِمْ رُسُلُهُم بِٱلْبَيِّنَـٰتِ فَكَفَرُوا۟ فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُ ۚ
إِنَّهُۥ قَوِىٌّ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ﴿23﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا مُوسَىٰ بِـَٔايَـٰتِنَا
وَسُلْطَـٰنٍ مُّبِينٍ ﴿24﴾ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ وَهَـٰمَـٰنَ وَقَـٰرُونَ
فَقَالُوا۟ سَـٰحِرٌ كَذَّابٌ ﴿25﴾ فَلَمَّا جَآءَهُم بِٱلْحَقِّ مِنْ عِندِنَا
قَالُوا۟ ٱقْتُلُوٓا۟ أَبْنَآءَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مَعَهُۥ وَٱسْتَحْيُوا۟
نِسَآءَهُمْ ۚ وَمَا كَيْدُ ٱلْكَـٰفِرِينَ إِلَّا فِى ضَلَـٰلٍ ﴿26﴾

ربع

16. A yau ne ake sakawa kowace kai da abindata aikata bazalin-ci a yau, haƙiƙa Ubangiji mai garajen sakamako ne. Zai yiwa halittarsa sakamako a cikin ra-bin rana na daga kwanukan duniya saboda hadisin daya faɗi haka).

(BAN TSORO GA KAFIRAI DA FIRGITASU)

17. Ka basu tsoron rana makusan-ciya (ranar Al¯iyama) zamanin da zukata take dakan uku-uku don tsoron nan ga maKogwarai suna hadiyar baƙin ciki.
18. Azzalumai basu da masoyi wala mai ceto da aka amsa masa (wato ba mai ceto garesu fau-fau).
19. Allah yasan ha'incin idonduna (wato satar duba izuwa abin ha-ramtawa, Allah yasan abinda Kiraza take boyewa).
20. Allah yana hukunci da gaskiya, waɗanda kuke bautawa (ku kafi-ran Makka ba Allah basune gumaka), basa hukunci da ko-mai (yaya zasu zama shaƙiƙai ga Ubangiji) haƙiƙa Ubangiji Shine mai ji mai gani (ga ma-ganganunsu da ayyukansu).
21. Shin bazasuyitafiya bane a cikin ƙasa su dubasu gani yaya ƙarshen waɗanda suke gabansu ya kasance sun kasance mafi tsanani daga garesu a wajen karfi da gurabu a cikin ƙasa (na daga tankuna na cikin rami na ruwa da gine-ginen katangu), Sai ubangiji ya halakar dasu sa-boda zunuban su, mai kiyaye su daga azabar Ubangiji bai ka-sance a garesu ba.
22. Wancanenka saboda cewa haƙiƙa cewa su manzannisu sun kasance suna zuwa musu da mu'ujizozi mabayyana, suka ka-firce, sai Ubangiji ya rike su (ma'ana ya halakar dasu), haƙiƙa shi Ubangiji mai karfi ne mai tsananin ukubane

(ƘISSAR ANNABI TAREDA FIR'AUNA DA HAMANA DA KARUNA DA MATSAYIN CIKAKKEN MUMINI)

23. Haƙiƙa mun aiko Annabi Musa da ayoyinmu da dalili mabayya-ni.
24. (Mun aiko shi) izuwa Fir'auna da Hamana da K.aruna sai sukace "Shi matsafi ne maƙaryaci".
25. To zamanin dayazo musu da gaskiya daga garemu sai sukace, "Ku kashe 'ya'yan waɗanda suka bada gaskiya tare dashi, ku wanzar da matayensu" kai-din Fir'auna bai kasance basai a cikin halaka.

وَقَالَ فِرْعَوْنُ ذَرُونِيَ أَقْتُلْ مُوسَىٰ وَلْيَدْعُ رَبَّهُۥٓ إِنِّيَ أَخَافُ
أَنْ يُّبَدِّلَ دِينَكُمْ وَأَنْ يُّظْهِرَ فِي الْأَرْضِ الْفَسَادَ (26) وَقَالَ مُوسَىٰٓ
إِنِّيَ عُذْتُ بِرَبِّي وَرَبِّكُم مِّن كُلِّ مُتَكَبِّرٍ لَّا يُؤْمِنُ بِيَوْمِ
الْحِسَابِ (27) وَقَالَ رَجُلٌ مُّؤْمِنٌ مِّنْ ءَالِ فِرْعَوْنَ يَكْتُمُ إِيمَانَهُۥٓ
أَتَقْتُلُونَ رَجُلًا أَنْ يَّقُولَ رَبِّيَ اللَّهُ وَقَدْ جَآءَكُم بِالْبَيِّنَٰتِ
مِن رَّبِّكُمْ وَإِنْ يَّكُ كَٰذِبًا فَعَلَيْهِ كَذِبُهُۥ وَإِنْ يَّكُ صَٰدِقًا
يُصِبْكُم بَعْضُ الَّذِي يَعِدُكُمُۥٓ إِنَّ اللَّهَ لَا يَهْدِي مَنْ هُوَ مُسْرِفٌ
كَذَّابٌ (28) يَٰقَوْمِ لَكُمُ الْمُلْكُ الْيَوْمَ ظَٰهِرِينَ فِي الْأَرْضِ
فَمَنْ يَّنصُرُنَا مِنۢ بَأْسِ اللَّهِ إِن جَآءَنَا قَالَ فِرْعَوْنُ
مَآ أُرِيكُمُۥٓ إِلَّا مَآ أَرَىٰ وَمَآ أَهْدِيكُمُۥٓ إِلَّا سَبِيلَ الرَّشَادِ (29)
۞ وَقَالَ الَّذِيٓ ءَامَنَ يَٰقَوْمِ إِنِّيَ أَخَافُ عَلَيْكُم مِّثْلَ يَوْمِ الْأَحْزَابِ (30) ثمن
مِثْلَ دَأْبِ قَوْمِ نُوحٍ وَعَادٍ وَثَمُودَ وَالَّذِينَ مِنۢ بَعْدِهِمْ
وَمَا اللَّهُ يُرِيدُ ظُلْمًا لِّلْعِبَادِ (31) وَيَٰقَوْمِ إِنِّيَ أَخَافُ
عَلَيْكُمْ يَوْمَ التَّنَادِ (32) يَوْمَ تُوَلُّونَ مُدْبِرِينَ مَا لَكُم
مِّنَ اللَّهِ مِنْ عَاصِمٍ وَمَنْ يُّضْلِلِ اللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِنْ هَادٍ (33)

26. Fir'auna yace "Ku barni in kashe Musa, (saboda su sun ka-sance zasu wadatar dashi ga buran kashe shi)[1] ya kira Ubangijinsa (domin ya hana shi daga gare ni), ni ina jin tsoro kada ya musanya muku addinin-ku (Kubi shi) kuma ina tsoron ya bayyana ɓama a bayan leasa (Shine kisa da waninsa").

27. Annabi Musa ya faɗa (ga muta-nensa alhali yaji wannan maga-na), "Ni na nemi tsari da Ubangijina da Ubangijinku daga dukkan mai girman kai wanda bai bada gaskiya da ranar lahira ba".

28. Sai wani mutum mumini daga makusantan Fir'auna da yake boyewan imaninsa sai yace, "yanzu kwa kashe mutum don kawai yana cewa "Ubangijina Allah?" Haƙiƙa yazo mukuda hujjoji mabayyana (sune mu'ujuzozi) daga Ubangijinku, in ya nce malearyaci to cut-ar Karyarsa tana kansa, in ya ka-sance magasgaci shashin abinda yake muku alkawari dashi (na azaba) saiya same ku a gag-gauce,. haƙiƙa Ubangiji bazai shiryi mushuriki mai yawan Karya ba.

29. "Yaku mutanena kuna da mulki a yau kuna masu rrnjaye a cikin ƙasar Misra to waye zai taimake mu daga azabar Ubangiji (inkun kashe waliyansa?) In azabar tazo mana (ba mai hana mana azabar), Fir'auna sai yace, "bana nuna muku sai abinda nake ishara dashi a kan kaina, (Shine kashe Annabi Musa), bana shi-riyar ku sai hanyar tsira".

30. Shi mutumin nan daya bada gaskiya dai yace "Ni ina jin tsoron misalin ranar kungiyoyi a gareku".

31. "Misalin halin mutanen Annabi Nuhu da Adu da Samadu da waɗanda suke bayansu, misalin (sakamakon al'adar wanda ya kafirta gaban ku na daga azabasu a duniya), Allah baya nufin zalinci ga bayinsa.

32. "Yaku mutanena ni ina jin tsoron ranar kiraye-kirayen juna (wato ranar lahira) a gareku ('yan wuta suna kiran 'yan aljanna, 'yan aljanna suna kiran yan wuta).

33. "Ranar da kuke juyawa kuna masu bada baya (daga matsayin hisabi izuwa wuta), bakuda mai hana muku (azabar Ubangiji) wanda Allah ya ɓatar dashi to ba mai shiryarwa a gareshi.

(1) Siyakin maganar yana nuna cewa suna nufin suyimasa wata ufcubana mai tsanani ba kisa ba, ya guji kadasu wadatada uRuba ga buran kashe shi, saboda haka yace su bar shi dashi, to wannan tawilin yana dacewa da tawi-lin farko wanda Shehu Sawi ya fadaShine cewa ARRAJULU MUMINU wand anbaton-sa zaizo cewa abokın asirin Fir'auna nc wanda ya kasancc yana yin dabara a cikin kashc shi, kuma yafi sauran ihtimalolin da-cewa wandaShine Ihtimalin farko kamar yadda Sawi ya fadayafi sauran ihtimalolin guda uku dacewa don an fahinto Shine da faɗin Ubangiji ZARUNI TA AMMAL dubada kyau, -Sanajiy-

وَلَقَدْ جَآءَكُمْ يُوسُفُ مِن قَبْلُ بِالْبَيِّنَٰتِ فَمَا زِلْتُمْ فِي شَكٍّ
مِّمَّا جَآءَكُم بِهِۦ حَتَّىٰٓ إِذَا هَلَكَ قُلْتُمْ لَن يَبْعَثَ اللَّهُ مِنۢ بَعْدِهِۦ
رَسُولًا كَذَٰلِكَ يُضِلُّ اللَّهُ مَنْ هُوَ مُسْرِفٌ مُّرْتَابٌ (34) الَّذِينَ
يُجَٰدِلُونَ فِيٓ ءَايَٰتِ اللَّهِ بِغَيْرِ سُلْطَٰنٍ اَتَىٰهُمْ كَبُرَ مَقْتًا
عِندَ اللَّهِ وَعِندَ الَّذِينَ ءَامَنُواْ كَذَٰلِكَ يَطْبَعُ اللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ
قَلْبٍ مُتَكَبِّرٍ جَبَّارٍ (35) وَقَالَ فِرْعَوْنُ يَٰهَٰمَٰنُ ابْنِ لِي
صَرْحًا لَّعَلِّيَ أَبْلُغُ الْأَسْبَٰبَ (36) أَسْبَٰبَ السَّمَٰوَٰتِ فَأَطَّلِعَ
إِلَىٰٓ إِلَٰهِ مُوسَىٰ وَإِنِّي لَأَظُنُّهُۥ كَٰذِبًا وَكَذَٰلِكَ زُيِّنَ
لِفِرْعَوْنَ سُوٓءُ عَمَلِهِۦ وَصَدَّ عَنِ السَّبِيلِ وَمَا كَيْدُ
فِرْعَوْنَ إِلَّا فِي تَبَابٍ (37) وَقَالَ الَّذِيٓ ءَامَنَ يَٰقَوْمِ
اِتَّبِعُونِي أَهْدِكُمْ سَبِيلَ الرَّشَادِ (38) يَٰقَوْمِ إِنَّمَا هَٰذِهِ
الْحَيَوٰةُ الدُّنْيَا مَتَٰعٌ وَإِنَّ الْأَخِرَةَ هِيَ دَارُ الْقَرَارِ (39)
مَنْ عَمِلَ سَيِّئَةً فَلَا يُجْزَىٰٓ إِلَّا مِثْلَهَا وَمَنْ عَمِلَ
صَٰلِحًا مِّن ذَكَرٍ اَوْ اُنثَىٰ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَأُوْلَٰٓئِكَ
يَدْخُلُونَ الْجَنَّةَ يُرْزَقُونَ فِيهَا بِغَيْرِ حِسَابٍ (40)

34. " Haƙiƙa Annabi Yusifu yazo muku tun gaban Annabi Musa (wato Shine Yusifu ɗan Ya'aƙubu yazo muku) da hujjoji mabayyana baku gushe ba cikin kokonto daga abinda yazo muku dashi har yayin daya ƙaura sai kukace (ba tareda wani dalili bakuka ce) "Allah bazai aiko wani manzo bayansa ba, (baku gushe kuna masu ƙaryatawa da Annabi Yusifu da waninsa ba) kamar yadda ya ɓatar daku ,yake ɓatar da wanda yake maɓarnaci (dashirka) maikokonto (cikin abinda mu'ujizozi mabayyana suka shaida dashi).

35. Waɗanda suke yin jayyaya cikin ayoyin Allah (wato mu ujizozinsa) ba tareda wani dalili dayazo musu ba, jayayyarsu ya girmama a wajen Ubangiji da gurin waɗanda suka bada gaskiya, kamar irin wannan ɓatarwa ne Allah yake yimkewa da ɓatawar a kan dukkan zuciyar mai girman kai da taƙadaranci.

36. Sai Fir'auna yace, "Ya kai Ha-manu gina mini soron bene maɗaukaki wata ƙila in isa sababai.

37. "Hanyoyin sammai dasuke kaiwa izuwa gareta donin yi tsinkaye izuwa Ubangijin Annabi Musa, haƙiƙa lallai ni ina zaton Annabi Musa maƙaryaci ne, (cikin cewa yana da Ubangiji bani ba. (Fir'auna ya faɗi wannan ne don jefawa a cikin wahami kuma don cuɗanyawa a cikin karya da gaskiya wato kasgare-wa), haƙana aka ƙawatawa Fir'auna mummunan aikinsa ya hana mutanensa bin hanyar gaskiya. Kaidin Fir'auna bai kasance ba face a cikin taɓewa.

38. Wanda ya bada gaskiya dai yace "Yaku mutanena", kubini in shiryeku tafarkin tsira".

39. Yace, "Yaku mutanena dahir dai wannan duniya ɗan ƙanƙanin anfani ce (da take gushewa), haƙiƙa lahira Itace gida tabbata.

40. Wanda ya aikata aiki mummuna baza a saka masa basaida mummuna kamarsa, wanda ya aikata aiki na gari daga namiji ko mace alhali shi yana mumini waɗancanenka zasu shiga aljanna, za a azurta su a cikinta bada ƙidaya ba.

حزب

* وَيَٰقَوْمِ مَا لِيَ أَدْعُوكُمْ إِلَى ٱلنَّجَوٰةِ وَتَدْعُونَنِيَ إِلَى ٱلنَّارِ ﴿41﴾
تَدْعُونَنِي لِأَكْفُرَ بِٱللَّهِ وَأُشْرِكَ بِهِۦ مَا لَيْسَ لِي بِهِۦ عِلْمٌ
وَأَنَا أَدْعُوكُمْ إِلَى ٱلْعَزِيزِ ٱلْغَفَّارِ ﴿42﴾ لَا جَرَمَ أَنَّمَا
تَدْعُونَنِي إِلَيْهِ لَيْسَ لَهُۥ دَعْوَةٌ فِي ٱلدُّنْيَا وَلَا فِي ٱلْأٓخِرَةِ
وَأَنَّ مَرَدَّنَا إِلَى ٱللَّهِ وَأَنَّ ٱلْمُسْرِفِينَ هُمْ أَصْحَٰبُ
ٱلنَّارِ ﴿43﴾ فَسَتَذْكُرُونَ مَا أَقُولُ لَكُمْ وَأُفَوِّضُ أَمْرِيَ
إِلَى ٱللَّهِ إِنَّ ٱللَّهَ بَصِيرٌۢ بِٱلْعِبَادِ ﴿44﴾ فَوَقَىٰهُ ٱللَّهُ سَيِّـَٔاتِ
مَا مَكَرُوا وَحَاقَ بِـَٔالِ فِرْعَوْنَ سُوٓءُ ٱلْعَذَابِ ﴿45﴾
ٱلنَّارُ يُعْرَضُونَ عَلَيْهَا غُدُوًّا وَعَشِيًّا وَيَوْمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ
أَدْخِلُوٓا ءَالَ فِرْعَوْنَ أَشَدَّ ٱلْعَذَابِ ﴿46﴾ وَإِذْ يَتَحَآجُّونَ
فِي ٱلنَّارِ فَيَقُولُ ٱلضُّعَفَٰٓؤُا لِلَّذِينَ ٱسْتَكْبَرُوٓا إِنَّا كُنَّا
لَكُمْ تَبَعًا فَهَلْ أَنتُم مُّغْنُونَ عَنَّا نَصِيبًا مِّنَ ٱلنَّارِ ﴿47﴾
قَالَ ٱلَّذِينَ ٱسْتَكْبَرُوٓا إِنَّا كُلٌّ فِيهَا إِنَّ ٱللَّهَ
قَدْ حَكَمَ بَيْنَ ٱلْعِبَادِ ﴿48﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ فِي ٱلنَّارِ لِخَزَنَةِ جَهَنَّمَ
ٱدْعُوا رَبَّكُمْ يُخَفِّفْ عَنَّا يَوْمًا مِّنَ ٱلْعَذَابِ ﴿49﴾

41. Yaku mutanena me ke gareni nake kiranku izuwa tsira kuke kirana izuwa wuta?.
42. Kuna kirana don in kafirtada Allah, in shirkanta dashi abinda bani da sani dashi, ni ko ina kiranku izuwa mabuwayi mai yawan gafara (ga wanda ya tuba).
43. Tabbas dahir dai abinda kuke kirana gareshi don in bauta masa bashi da amsa roƙo a duniya wala a lahira, haƙiƙa mak-omarmu yana ga Allah, haƙiƙa kafirai su ne'yan wuta.
44. Da sannu zaku tuna abinda nake gaya muku (inkun ga azabar Ubangiji) ina zuba al'amarina izuwa Allah, haƙiƙa Ubangiji masanine da bayinsa, (ya faɗa musu zamanin da sukayi masa narko da saɓawar addininsu, da suka fahimce shi a tareda Annabi Musa yake).
45. Sai Ubangiji ya kiyashe shi miyagun abinda sukayi nufi dashi (na daga kisa), mummunar azabata sauko ga Fir'auna da mutanensa (nitsewa).
46. (Sannan kuma) wuta ana bijirar dasu a kanta safiya dayammaci, kuma ranar da alƙiyama take tsayawa (ana cewa) ku shigar da Fir'auna da mutanensa mafi tsananin azaba.

(WANI ABU DAGA MATSAYIN KAFIRAI A DUNIYA DA LAHIRA)

47. Ka ambata zamanin da kafirai suke husuma a cikin wuta raunana su faɗa ga waɗannan dasuke jin girma, "Haƙiƙa mu mun kasance mabiyagareku, to shin ku masu ije mana wani yanki na wuta ne ga buran mu".
48. Sai masu jin girma su ce, "Lallai mu dukkan mu muna cikinta, haƙiƙa Allah yayi hukunci tsakanin bayinsa, (ya shigar da muminai aljanna, kafirai wuta").
49. Waɗanda suke cikin wuta suka faɗa ga mataskata jahannama, "Ku roƙi Ubangijinku ya sauwaƙe mana gwargwadon wuni ɗaya na azaba ga buran mu".

قَالُوٓاْ أَوَلَمۡ تَكُ تَأۡتِيكُمۡ رُسُلُكُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِۖ قَالُواْ بَلَىٰۚ
قَالُواْ فَٱدۡعُواْۗ وَمَا دُعَٰٓؤُاْ ٱلۡكَٰفِرِينَ إِلَّا فِي ضَلَٰلٍ ﴿50﴾
إِنَّا لَنَنصُرُ رُسُلَنَا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَيَوۡمَ
يَقُومُ ٱلۡأَشۡهَٰدُ ﴿51﴾ يَوۡمَ لَا يَنفَعُ ٱلظَّٰلِمِينَ مَعۡذِرَتُهُمۡۖ
وَلَهُمُ ٱللَّعۡنَةُ وَلَهُمۡ سُوٓءُ ٱلدَّارِ ﴿52﴾ ۞ وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا
مُوسَى ٱلۡهُدَىٰ وَأَوۡرَثۡنَا بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱلۡكِتَٰبَ ﴿53﴾ هُدٗى
وَذِكۡرَىٰ لِأُوْلِي ٱلۡأَلۡبَٰبِ ﴿54﴾ فَٱصۡبِرۡ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞ
وَٱسۡتَغۡفِرۡ لِذَنۢبِكَ وَسَبِّحۡ بِحَمۡدِ رَبِّكَ بِٱلۡعَشِيِّ وَٱلۡإِبۡكَٰرِ ﴿55﴾
إِنَّ ٱلَّذِينَ يُجَٰدِلُونَ فِيٓ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ بِغَيۡرِ سُلۡطَٰنٍ
أَتَىٰهُمۡ إِن فِي صُدُورِهِمۡ إِلَّا كِبۡرٞ مَّا هُم بِبَٰلِغِيهِۚ
فَٱسۡتَعِذۡ بِٱللَّهِۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ ﴿56﴾ لَخَلۡقُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ أَكۡبَرُ مِنۡ خَلۡقِ ٱلنَّاسِ
وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ﴿57﴾ وَمَا
يَسۡتَوِي ٱلۡأَعۡمَىٰ وَٱلۡبَصِيرُ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ
ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَلَا ٱلۡمُسِيٓءُۚ قَلِيلٗا مَّا تَتَذَكَّرُونَ ﴿58﴾

ثمن

50. Sai mataskata suka faɗa (don ba'a), Shin manzanninku basu kasance suna zuwa mukuda hujjoji mabayyana da (mu'ujizozi mabayyana) bane?" Sukace sun zo mana da ita (suka kafirce da manzannin) sukace, "Ku roƙe shi, (saboda mu Barna ceto ga kafiri in ji manzanni sai Ubangiji ta'ala yace), Addu'ar kafirci bata kasance basai a cikin ɓata".
51. (Yaci gabada cewa) " Haƙiƙa mumuna taimakon manzanninmu da waɗanda suka bada gaskiya a rayuwar duniya da ranar da shaidu zasu miƙe tsaye (sune Mala'iku, su shaidar da iyar da aike ga manzanni, su shaidar da ƙaryatawa ga kafirai).
52. Ranar da hanzarin azzalimai bazai anfane su ba (da zasuyihanzarin), haƙiƙa la'ana (nisata ga buran rahama) tana garesu, suna da mummunan gida (Shine tsanin azaba a lahira).
53. Haƙiƙa mun baiwa Annabi Musa shiriya (wato Attaura mu'ujizozi), mun gadewa bani Isra'ila Attaura bayan Annabi Musa, mai shiriya, mai gargaɗi ga ma'abota hankula.
54. Saboda haka sai ka daure (ya Annabi Sallallahu alaika wa sallama), haƙiƙa alkawarin taimakon waliyansa gaskiya ne, kai salla kana mai haɗawa da godiyar Ubangijinka dayammaci da safiya (sune salloli guda biyar).

(JAYAYYA CIKIN AYOYIN ALLAH DA SABABINSA TAREDA ANBATON BA'ALIN NI'IMOMI)

55. Haƙiƙa waɗannan dasuke jayayya cikin ayoyin Allah (Alƙur'ani) ba tareda wani dalili dayazo muzu ba, ba wani abu cikin ƙirazansu saitakabburanci (da tammaha su hau kanka), su bazasu riski wannan ba, ka nemi taimako da Allah (daga sharrin su), Ubangiji haƙiƙa Shine mai ganin (maganganunsu mai gani ga haluluwansu). (Wannan aya ta sauka a cikin masu musun alƙiyama).
56. Lallai halittar sammai da ƙassai (da farko) Shine yafi halittar mutane (marra ta biyu, wato Itace mai dasu rayayyu), saidai yawancin mutane (kafiran Mak-ka) basu san wannan ba. (Su kamar makaho suke, wanda yasan wannan kamar mai ido ne).
57. Makaho da mai ido bazasuyidaidai ba.
58. Wala waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru, (wato Shine mai kyautatawa) wala mai munanawa (bazai daidai da wanda yayi kyakykyawan aiki ba), kaɗan ne ƙwarai kuke wa'azantuwa.

إِنَّ ٱلسَّاعَةَ لَءَاتِيَةٌ لَّا رَيْبَ فِيهَا وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿59﴾
وَقَالَ رَبُّكُمُ ٱدْعُونِيَ أَسْتَجِبْ لَكُمْ إِنَّ ٱلَّذِينَ
يَسْتَكْبِرُونَ عَنْ عِبَادَتِي سَيَدْخُلُونَ جَهَنَّمَ دَاخِرِينَ ﴿60﴾
ٱللَّهُ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلَّيْلَ لِتَسْكُنُوا فِيهِ وَٱلنَّهَارَ مُبْصِرًا
إِنَّ ٱللَّهَ لَذُو فَضْلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ
لَا يَشْكُرُونَ ﴿61﴾ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمْ خَٰلِقُ كُلِّ شَيْءٍ
لَّا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَأَنَّىٰ تُؤْفَكُونَ ﴿62﴾ كَذَٰلِكَ يُؤْفَكُ
ٱلَّذِينَ كَانُوا بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ يَجْحَدُونَ ﴿63﴾ ٱللَّهُ ٱلَّذِي
جَعَلَ لَكُمُ ٱلْأَرْضَ قَرَارًا وَٱلسَّمَآءَ بِنَآءً وَصَوَّرَكُمْ
فَأَحْسَنَ صُوَرَكُمْ وَرَزَقَكُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ
ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمْ فَتَبَارَكَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿64﴾
هُوَ ٱلْحَيُّ لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَٱدْعُوهُ مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ
ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿65﴾ * قُلْ إِنِّي نُهِيتُ أَنْ أَعْبُدَ ربع
ٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ لَمَّا جَآءَنِيَ ٱلْبَيِّنَٰتُ
مِن رَّبِّي وَأُمِرْتُ أَنْ أُسْلِمَ لِرَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿66﴾

59. Lallai alƙiyama mai zuwa ce ba kokwanto a cikinta, amma yawancin mutane basu bada gaskiya (da ita) ba.

(FALALAR ADDU'A)

60. Ubangijinku yace, "Ku roƙe ni na amsa muku (ai ku bautamin) in yi muku sakamako, haƙiƙa waɗanda suke girman kai ga buran bautatada sannu zasu shiga jahannama suna wulaƙance.
61. Allah Shine wanda yasanya muku dare domin ku nutsu a cikinsa, yasanya muku rana mai tangarewa, haƙiƙa Ubangiji ma'abocin falala ne bisa mu-tane, saidai yawancin mutane basa godewa Allah.
62. Wancanenku Shine Allah Ubangijinku mahaliccin komai, ba abin bautawa da gaskiya sai shi, yaya ake juyar daku ,(ga buran imani tareda tsayawar burhani).
63. Tamfar da aka juyar da waɗannan hakana aka juyar da waɗanda suka kasance suna musun ayoyin Allah (wato mu'ujizozinsa).
64. Allah ne wanda yasanya ƙasa matabbaci a gareku, yasanya sama rifi,ya suranta ku a mahaifa, ya kyautata surorinku, ya azurta ku daga dadddan halalai wancanenku Allah ne Ubangijinku to madalla Allah Ubangi-jin talikai.
65. Shine rayayye, babu abin bautawa da gaskiya sai shi, ku bauta masa kuna tsarkakewar addini gareshi (daga shirka), godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai.

(YAYA AKE BAUTAWA WANIN ALLAH)

66. Cene, "Ni haƙiƙa an hane ni in bautawa abinda kuke bautawa ba Allah ba yayin da hujjoji (na tauhidi) sukazo mini daga Ubangijina an umarce ni in miƙa wuyaga Ubangijin talikai.

هُوَ ٱلَّذِي خَلَقَكُم مِّن تُرَابٖ ثُمَّ مِن نُّطْفَةٖ ثُمَّ مِنْ عَلَقَةٖ
ثُمَّ يُخْرِجُكُمْ طِفْلٗا ثُمَّ لِتَبْلُغُوٓاْ أَشُدَّكُمْ ثُمَّ لِتَكُونُواْ شُيُوخٗاۚ
وَمِنكُم مَّن يُتَوَفَّىٰ مِن قَبْلُۖ وَلِتَبْلُغُوٓاْ أَجَلٗا مُّسَمّٗى
وَلَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿67﴾ هُوَ ٱلَّذِي يُحْيِۦ وَيُمِيتُۖ فَإِذَا قَضَىٰٓ
أَمْرٗا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ﴿68﴾ أَلَمْ تَرَ
إِلَى ٱلَّذِينَ يُجَٰدِلُونَ فِيٓ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ أَنَّىٰ يُصْرَفُونَ ﴿69﴾
ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِٱلْكِتَٰبِ وَبِمَآ أَرْسَلْنَا بِهِۦ رُسُلَنَاۖ فَسَوْفَ يَعْلَمُونَ ﴿70﴾
إِذِ ٱلْأَغْلَٰلُ فِيٓ أَعْنَٰقِهِمْ وَٱلسَّلَٰسِلُ يُسْحَبُونَ فِي ٱلْحَمِيمِ ﴿71﴾
ثُمَّ فِي ٱلنَّارِ يُسْجَرُونَ ﴿72﴾ ثُمَّ قِيلَ لَهُمْ أَيْنَ مَا كُنتُمْ
تُشْرِكُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِۖ قَالُواْ ضَلُّواْ عَنَّا بَل لَّمْ نَكُن
نَّدْعُواْ مِن قَبْلُ شَيْـٔٗاۚ كَذَٰلِكَ يُضِلُّ ٱللَّهُ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿73﴾ ذَٰلِكُم
بِمَا كُنتُمْ تَفْرَحُونَ فِي ٱلْأَرْضِ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ وَبِمَا كُنتُمْ تَمْرَحُونَ ﴿74﴾
ٱدْخُلُوٓاْ أَبْوَٰبَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَاۖ فَبِئْسَ مَثْوَى
ٱلْمُتَكَبِّرِينَ ﴿75﴾ فَٱصْبِرْ إِنَّ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقّٞۚ فَإِمَّا نُرِيَنَّكَ بَعْضَ
ٱلَّذِي نَعِدُهُمْ أَوْ نَتَوَفَّيَنَّكَ فَإِلَيْنَا يُرْجَعُونَ ﴿76﴾

67. "Shine wanda ya halicce ku daga turɓaya da haliftar ubanku Annabi Adamu daga gareshi sannan daga nuɗafa (Shine ɗigon ƙazanta), sannan daga gudan jini, sannan yafitar daku ,jirajirai, sannan ya wanzar daku ,domin ku isa cikar ƙarfinku (Shine daga 30-40), sannan don ku zamo tsofaffi, akwai daga cikin ku wanda ake karɓarsa tun ga-ban cikar ƙarfinsa da tsufa (yana aikata wannan daku ,don ku rayu) kuma don ku isa ajali abin ambato watakila kwa hankaƙi (dalilan tauhidi ku bada gaskiya).
68. Shine wanda yake rayawa yake matarwa idan yanufi samar da al'amari sai kawai yace dashi, "Samu" saiya mu.

(MASUJIDALI DA SAKAMAKONSU DA HAƘURIN ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAMA BISA CUTARSU)

69. Shin bakayi duba bane izuwa waɗannan dasuke jayayya a cikin ayoyin Allah (wato alƙur'ani) yaya ake juyar dasu (ga buran imani?).
70. Waɗanda suka ƙaryatada alƙur'ani da abinda muka aiko manzanninmu dashi (na tauhidi da tashin alƙiyama) da sannu zamu san (uƙubar ƙaryatawarsu).
71. Zamanin daƙuƙumai suke wuyayinsu, sarƙoƙi kuma suke ƙafafuwansu ana jan su (da ita) izuwa wutar jahannama.
72. Sannan a babbaka su a cikin wutar jahannama.
73. Sannan a ce dasu ina abinda kuka kasance kuna shirkantawa ba Allah ba (sune gumaka), saisu ce sun guje mana (Barna ganin su), kai mu bamu kasance muna bautawa komai a da can ba. (Sun yi musun bauta mata sannan aka kawo su gumakan. Ubangiji ta'ala yacc, " haƙiƙa kuda abinda kuke bautawa ba Allah ba, gumaguman jahannama ne ku). Kamar yadda muka ɓatar da masu ƙaryatawa, Allah yake ɓatar da kafirai (ana cewa dasu har yau).
74. Wacanenku azabasaboda kun kasance kuna farin ciki ne a cikin ƙasa bada gaskiyaba (Shine shirka da musun tashin alƙiyama), saboda kuma kun kasance kuna yin galla.
75. Ku shiga ƙofin jahannama kuna masu dauwama a cikinta, to tir makomar masu girman kai.
76. Ka daure ka haƙura haƙiƙa alƙawarin Allah (da azabarsa) gaskiya ne, haƙiƙa to in muka nuna maka shashin abinda muke musu alwashi dashi (na azaba, a rayuwarka, to shi ke nan), ko muka karɓi ranka (gaban bamu yi musu azaba ba) to izuwa garetnu zasu koma, mu ɗanɗana musu azaba mafi tsananin azaba.

وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا رُسُلًا مِّن قَبْلِكَ مِنْهُم مَّن قَصَصْنَا عَلَيْكَ
وَمِنْهُم مَّن لَّمْ نَقْصُصْ عَلَيْكَ وَمَا كَانَ لِرَسُولٍ أَن يَأْتِيَ
بِـَٔايَةٍ إِلَّا بِإِذْنِ اللَّهِ فَإِذَا جَاءَ أَمْرُ اللَّهِ قُضِيَ بِالْحَقِّ
وَخَسِرَ هُنَالِكَ الْمُبْطِلُونَ ﴿77﴾ ۞ اللَّهُ الَّذِي جَعَلَ ثمن
لَكُمُ الْأَنْعَامَ لِتَرْكَبُوا مِنْهَا وَمِنْهَا تَأْكُلُونَ ﴿78﴾ وَلَكُمْ
فِيهَا مَنَافِعُ وَلِتَبْلُغُوا عَلَيْهَا حَاجَةً فِي صُدُورِكُمْ وَعَلَيْهَا
وَعَلَى الْفُلْكِ تُحْمَلُونَ ﴿79﴾ وَيُرِيكُمْ ءَايَاتِهِ فَأَيَّ ءَايَاتِ اللَّهِ
تُنكِرُونَ ﴿80﴾ أَفَلَمْ يَسِيرُوا فِي الْأَرْضِ فَيَنظُرُوا كَيْفَ كَانَ
عَاقِبَةُ الَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ كَانُوا أَكْثَرَ مِنْهُمْ وَأَشَدَّ قُوَّةً
وَءَاثَارًا فِي الْأَرْضِ فَمَا أَغْنَىٰ عَنْهُم مَّا كَانُوا يَكْسِبُونَ ﴿81﴾
فَلَمَّا جَاءَتْهُمْ رُسُلُهُم بِالْبَيِّنَاتِ فَرِحُوا بِمَا عِندَهُم مِّنَ الْعِلْمِ
وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُوا بِهِ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿82﴾ فَلَمَّا رَأَوْا بَأْسَنَا
قَالُوا ءَامَنَّا بِاللَّهِ وَحْدَهُ وَكَفَرْنَا بِمَا كُنَّا بِهِ مُشْرِكِينَ ﴿83﴾
فَلَمْ يَكُ يَنفَعُهُمْ إِيمَانُهُمْ لَمَّا رَأَوْا بَأْسَنَا سُنَّتَ اللَّهِ
الَّتِي قَدْ خَلَتْ فِي عِبَادِهِ وَخَسِرَ هُنَالِكَ الْكَافِرُونَ ﴿84﴾

77. Haƙiƙa mun aiko jakadu gabanka, akwai daga cikinsu waɗanda muka labarta maka (al'amarinsu), akwai daga cikinsu waɗanda bamu labarta maka komai na labarin su ba, an ruwaito cewa Ubangiji ya aiko Annabi Dubu takwas (8,000) ɗubu huɗu na bani Isra'ila, (4,000) dubu hudu na sauran mutane (4,000)[1] bazai yiwu ga wani manzo yazoda aya ba, saida izinin Allah, (saboda su bayi ne ababan mallakar Allah), idan al'amarin Allah yazo (da saukar azabar kafirai), sai ayi hukunci (tsakanin manzanni da masu ƙaryata su) da gaskiya, maƙaryata sun taɓe a canenka, (da ma su taɓaɓɓu ne a kowane lokaci gaban wancanenka).

(SHASHIN AYOYIN ALLAH DA NI'IMOMINSA A GAREMU)

78. Ubangiji ne wanda yasanya muku dabbobi (raƙuma da shanu da tumakai) domin ku hau daga gareta, kuma kuna ci daga gareta.

79. Kuna da anfanunuwa a cikinta (Shine nono da 'ya'ya da gashin zomaye wato gashi mai yalolo) don ku isa bukatada take cikin ƙirazan ku a kanta (Itace ɗaukanta izuwa gamruwa) ana ɗauke daku ,a cikin kogi ana ɗauke daku ,a kan jirgi a cikin sarari ana ɗauke daku ,a cikin jirage.

(MANYAN WALIYAI KAMAR SHEHU ABDULƘADIR JILANI DA SHEHU SHAZALI DA IZZUDOIN IBNI ABDUSSAMI DA SAURAN IRINSU DA MALAMAI MASU TSORON ALLAH, SANNAN DA BABUBURA, BASUKURA, JIRGIN SAMA DA SAURAN IRINSU A DUKKAN FILLIN DUNIYA)

80. Yana nuna muku ayoyinsa, to wacce ce daga ayoyin Allah kuke musu, (Amsa Barna musun ko ɗaya).

(BAN TSORO GA MASUJIDALI A CIKIN AYOYIN ALLAH)

81. Shin basuyitafiya bane a cikin ƙasa, su dubasu ga yaya ƙarshen waɗanda suke gabansu ya kasance? Sun kasance mafiya yawa daga garesu, sun fi su tsananin ƙarfi, sun fi su aikace-aikace a cikinsu (tankokin ruwa na ƙasa da benaye). Abinda suke tsoro baiwadatar musu da komai ba, (na daga azabar Allah).

82. Zamanin da jakadunsu sukazo musu da hujjoji na gaskiya sai sukayi izgili da abinda yake gurin manzanni na ilimi, suka ɓarke da dariya, abinda suka kasance suna izgili dashi (na azaba) ya sauka a garesu.

83. Yayin da suka ga ban kashinmu sai sukace, "mun bada gaskiya da Allah shi kaɗai, mun kafirce da abinda muka kasance muna shirkantawa dashi".

84. To imani nasu bai kasance zai anfane su bazamanin da suka ga tsananin azabarmu, wannan abu Allah ya sunnatashine sun-natawarsa, (wato Ya sanyashine al'ada tasa, wacce haƙiƙa ta wuce a cikin bayinsa (cewa imani bazai anfani ba lokacin azaba), kafirai taɓewarsu ta bayyana (a idanun kowa da ma su taɓaɓɓu ne a cananka).

1) Sawi yace ingantaccen abinda aka rowaito ga Abi Zarri yace, "Ya Rasulallahi nawa ne Icirgar Annabawa?" yace, "(Duhu dari da dubi ishirin da hudu (124,000) jakadu daga cikinsu Dari ukuda goma sha biyar (315) a taro mai yawa" -Sawi. An yi bayanin Ishirin da biyar (25) a cikin Alƙur'ani -Sawi.

41 سُورَةُ فُصِّلَتْ مَكِّيَّة

وَهِيَ ثَلَاثٌ وَخَمْسُونَ ءَايَة 53

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

حمٓ تَنزِيلٞ مِّنَ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ (1) كِتَٰبٞ فُصِّلَتۡ ءَايَٰتُهُۥ قُرۡءَانًا عَرَبِيّٗا
لِّقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ (2) بَشِيرٗا وَنَذِيرٗا فَأَعۡرَضَ أَكۡثَرُهُمۡ فَهُمۡ
لَا يَسۡمَعُونَ (3) وَقَالُواْ قُلُوبُنَا فِيٓ أَكِنَّةٖ مِّمَّا تَدۡعُونَآ إِلَيۡهِ
وَفِيٓ ءَاذَانِنَا وَقۡرٞ وَمِنۢ بَيۡنِنَا وَبَيۡنِكَ حِجَابٞ فَٱعۡمَلۡ إِنَّنَا عَٰمِلُونَ (4)
قُلۡ إِنَّمَآ أَنَا۠ بَشَرٞ مِّثۡلُكُمۡ يُوحَىٰٓ إِلَيَّ أَنَّمَآ إِلَٰهُكُمۡ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞ فَٱسۡتَقِيمُوٓاْ
إِلَيۡهِ وَٱسۡتَغۡفِرُوهُۗ وَوَيۡلٞ لِّلۡمُشۡرِكِينَ (5) ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ
وَهُم بِٱلۡأٓخِرَةِ هُمۡ كَٰفِرُونَ (6) إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
لَهُمۡ أَجۡرٌ غَيۡرُ مَمۡنُونٖ (7) ۞ قُلۡ أَئِنَّكُمۡ لَتَكۡفُرُونَ بِٱلَّذِي خَلَقَ ٱلۡأَرۡضَ ربع
فِي يَوۡمَيۡنِ وَتَجۡعَلُونَ لَهُۥٓ أَندَادٗاۚ ذَٰلِكَ رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ (8) وَجَعَلَ
فِيهَا رَوَٰسِيَ مِن فَوۡقِهَا وَبَٰرَكَ فِيهَا وَقَدَّرَ فِيهَآ أَقۡوَٰتَهَا فِيٓ أَرۡبَعَةِ
أَيَّامٖ سَوَآءٗ لِّلسَّآئِلِينَ (9) ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰٓ إِلَى ٱلسَّمَآءِ وَهِيَ دُخَانٞ
فَقَالَ لَهَا وَلِلۡأَرۡضِ ٱئۡتِيَا طَوۡعًا أَوۡ كَرۡهٗا قَالَتَآ أَتَيۡنَا طَآئِعِينَ (10)

Wannan Suratul Fussilati

A Makka aka saukar da ita Aya Hamsin da Uku ce (53)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a lahira a keɓe

Wannan Sura Ta Kunshi Zance A kan Alƙur'ani Da Matsayin Mushurkai Daga Alƙur'ani Da Ikon Allah A Cikin Halittar Sammai Da kassai, Da Ban Tsoro Ga Mushurikai Da Misalin Abinda ya Sauka Ga Adu Da Samudu Da Ban Tsoro Garesu Da Abindazai Tabbata Garesu Ranar Alƙiyama da Zance kan Cikakkun Muminai Da Bayanin ƙarshensu A Duniya Da Lahira Da Anbaton Ba'alin Ta'adodin Su.

(ALƘUR'ANI DA MATSAYIN MUSHURIKAI DAGA GARA SHI)

1. Allahu a'alamu bi muradihi bi zalika, Saukarwa daga Sarki mai jinƙai da manya-manyan ni'imomi da ƙananansu.
2. (Shine) littafi da aka fayyace ayoyinsa, (wato aka bayyanatada hukunce-hukunce da ƙissoshi da gargaɗe-gargaɗe) halin kasancewar wannan littafi Kur'anine Balarabe, ga mutane waɗanda sukasan wannan (sune Larabawa, saboda alƙur'ani da lugar sune amma waninsu bazai fa-himci alƙur'ani ba, saida wasiɗarsu).
3. Yana mai albishir, yana mai gargadi, to sai yawancinsu sukabijire, to su basajin sajin karɓa.
4. To suka faɗa (ga Annabi Sallallahu alaihi wa sallama) "Zukatanmu suna cikin rufe-rufe daga abinda kake kiranmu izuwa ga-reshi akwai shamaki tsakaninmu da kai, (Shine saɓani cikin addini) sai kayi aiki (kan addininka), muna haƙiƙa zamuyi aiki (kan addininmu).
5. Cene, "Dahir dai ni mutumne kamar ku ake aikowa izuwa gareni, haƙiƙa cewa Ubangijinku Allah ne guda (ɗayakuyi daidai izuwa gareshi (da imani) ku nemi gafararsa, ɗanɗana kuɗar azabata tabbata ga mushurikai.
6. Waɗanda basa bada zakka, su sun kafirce da ranar Lahira.
7. Haƙiƙa waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru lada dauwamamme ya tabbata garesu.

(ALLAH SHINE MAI IKO MAI NUFI)

8. Cene, "Yanzu ku kwa karfice da wanda halicci sammai da ƙassai a cikin mmiƙidarin kwana biyu (Lahadi da litinin). Kwa dunga sawan kinnai (wato sharikai a gareshi? Wancanenka Shine mana llakin talikai duk gaba ɗaya.
9. Yasanya muku duwarwatsu matabbata a cikinta, daga burbushinta yayi albarka a cikinta (da yawan ruwa da hantsotsi na nono) ya ƙaddara abincinta a cikinta (na mutane da dabbobin su, ya raba abincinta ga mutane da dabbobi) a cikin cikar kwana huɗu (a cikin Talatada Laraba) daidai wa daida ga masu tambayo (game da halittar ƙasa da abinda yake cikinsa).
10. Sannan yayi nufi izuwa sama alhali tana hayaƙi (wanda yayi sama dashi) yace da ƙasa da sama "Ku samu daidai dayadda nake nufi daga gareku girma da azziki ko tilas", sukace "Mun samu girma da azziki".

فَقَضَاهُنَّ سَبْعَ سَمَاوَاتٍ فِي يَوْمَيْنِ وَأَوْحَىٰ فِي كُلِّ سَمَاءٍ أَمْرَهَا
وَزَيَّنَّا السَّمَاءَ الدُّنْيَا بِمَصَابِيحَ وَحِفْظًا ذَٰلِكَ تَقْدِيرُ الْعَزِيزِ الْعَلِيمِ ﴿١١﴾
فَإِنْ أَعْرَضُوا فَقُلْ أَنذَرْتُكُمْ صَاعِقَةً مِّثْلَ صَاعِقَةِ
عَادٍ وَثَمُودَ ﴿١٢﴾ إِذْ جَاءَتْهُمُ الرُّسُلُ مِن بَيْنِ أَيْدِيهِمْ وَمِنْ خَلْفِهِمْ
أَلَّا تَعْبُدُوا إِلَّا اللَّهَ قَالُوا لَوْ شَاءَ رَبُّنَا لَأَنزَلَ مَلَائِكَةً فَإِنَّا بِمَا
أُرْسِلْتُم بِهِ كَافِرُونَ ﴿١٣﴾ فَأَمَّا عَادٌ فَاسْتَكْبَرُوا فِي الْأَرْضِ
بِغَيْرِ الْحَقِّ وَقَالُوا مَنْ أَشَدُّ مِنَّا قُوَّةً أَوَلَمْ يَرَوْا
أَنَّ اللَّهَ الَّذِي خَلَقَهُمْ هُوَ أَشَدُّ مِنْهُمْ قُوَّةً وَكَانُوا
بِآيَاتِنَا يَجْحَدُونَ ﴿١٤﴾ فَأَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ رِيحًا صَرْصَرًا فِي أَيَّامٍ
نَّحِسَاتٍ لِّنُذِيقَهُمْ عَذَابَ الْخِزْيِ فِي الْحَيَاةِ الدُّنْيَا وَلَعَذَابُ الْآخِرَةِ
أَخْزَىٰ وَهُمْ لَا يُنصَرُونَ ﴿١٥﴾ * وَأَمَّا ثَمُودُ فَهَدَيْنَاهُمْ فَاسْتَحَبُّوا
الْعَمَىٰ عَلَى الْهُدَىٰ فَأَخَذَتْهُمْ صَاعِقَةُ الْعَذَابِ الْهُونِ بِمَا كَانُوا
يَكْسِبُونَ ﴿١٦﴾ وَنَجَّيْنَا الَّذِينَ آمَنُوا وَكَانُوا يَتَّقُونَ ﴿١٧﴾ وَيَوْمَ
يُحْشَرُ أَعْدَاءُ اللَّهِ إِلَى النَّارِ فَهُمْ يُوزَعُونَ ﴿١٨﴾ حَتَّىٰ إِذَا مَا جَاءُوهَا
شَهِدَ عَلَيْهِمْ سَمْعُهُمْ وَأَبْصَارُهُمْ وَجُلُودُهُم بِمَا كَانُوا يَعْمَلُونَ ﴿١٩﴾

ثمن

11. Saiya mai da ita sammai guda bakwai a cikin miƙidarin kwana biyu (alhmis dajuma'a yagama daga gareta a cikin ƙarshen sa'a cikinta ya halicci Annabi Adamu[1] saboda haka bai ce Sawa'an ba, wannan aya tayi daidai da sauran ayoyin dasuke cewa an halicci sammai da ƙassai a kwana shida), ya aikowa da kowace sama al'amarinta (wanda ya umarci wanda yake cikinta dashi na ɗa'a da ibada), muka ƙawata saman duniya da taurari muka kiyayeta (daga satar ji wanda shaiɗanu suke yi), wancanenka Shine gwargwadawar mabuwayi (a cikin mulkinsa) masani (da halittarsa).

(FIRGITA SU DA ABINDA YA SAUKA GA ADU DA SAMUDU A DUNIYA)

12. To idan kafiran Makkah sun bijire (ga buran gaskiya bayan wannan bayani) to cene (dasu) "Na firgitar daku ,da tsawa misalin tsawar Adu da Samudu.

13. "Zamanin da jakadu sukazo musu nan tsakanin hanneyen su, (ai azabazata halakar daku kamar wacce ta halakar dasu, daga tsakanin hannayensu) da wajen bayansu, (wato suna masu fuskantowa garesu masu bada bayaga buransu, suka karfice. Halakarwar ta afkune saboda cewa) kadaku ,bautawa kowa sai Allah, sai sukace "Da Ubangiji ya nufa da saiya saukar da Mala'iku a kanmu, haƙiƙa mu mun kafirce da abinda aka aikoku dashi".

14. Amma Adu sunyi girman kai a bayan ƙasa bada gaskiya ba,sukace zamanin da aka basu tsoro da azaba), "Wanene yafimu tsananin ƙarfi?" (Babu, ɗayansu ya kasance yana ɓaɓɓake fa babbaya ajiyeta a indayaga dama), shin basu sani bane cewa haƙiƙa Allah wanda ya halicce su shine wanda yafisu tsananin ƙarfi, sun kasance suna musu da ayoyinmu.

15. Sai muka aiko iska a kansu mai tsananin sanyi (bada ruwa ba), a cikin kwanuka na NAHISA donmu ɗanɗana musu azabar kunyata a rayuwar duniya, lallai kuma azabar lahira tafi tsananin kunyata, su baza a hanasu (ga buran saɓa).

16. Amma Samudu to mun shiryesu hanyar gaskiya, sai suka zaɓi makanta (wato kafirci), a kan shiriya, sai tsawar. azaba mai wulaƙantawa ta riƙesu saboda abubuwan dasuke aikatawa.

17. Muka tserar da waɗanda suka bada gaskiya suka kasance suna tsoron Allah, daga gareta.

(FIRGITASU DA AZABA RANAR ALƘIYAMA)

18. Ambaci ranar da muke tara maƙiya Allah to su ana kora u (izuwa wuta).

19. Har yayinda sukazo mata sai kunnuwansu da idanunsu da fatunsu suka shaida a garesu da abinda suka kasance suna aikatawa.

1) A cikin sa'ata karshe aka halicci Annabi Adamu amma ba Annabi adamu na mu ba, Annabi adamu na farko abinda bincike ya nuna cewa wannan Shine Adamu na farko, Adamu namu Shine na Rarshe, a tsakanin Adamu na farko dana Karshe akwai Adamomi da yawa kamar yadda bincike ya nuna. -Sanajiy-

وَقَالُواْ لِجُلُودِهِمْ لِمَ شَهِدتُّمْ عَلَيْنَا قَالُوٓاْ أَنطَقَنَا اَللَّهُ اُلَّذِيٓ أَنطَقَ
كُلَّ شَيْءٍ وَهْوَ خَلَقَكُمْ أَوَّلَ مَرَّةٍ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿20﴾
وَمَا كُنتُمْ تَسْتَتِرُونَ أَنْ يَّشْهَدَ عَلَيْكُمْ سَمْعُكُمْ
وَلَآ أَبْصَارُكُمْ وَلَا جُلُودُكُمْ وَلَٰكِن ظَنَنتُمُوٓ أَنَّ اَللَّهَ لَا يَعْلَمُ
كَثِيراً مِّمَّا تَعْمَلُونَ ﴿21﴾ وَذَٰلِكُمْ ظَنُّكُمُ اُلَّذِي ظَنَنتُم بِرَبِّكُمْ
أَرْدَىٰكُمْ فَأَصْبَحْتُم مِّنَ اَلْخَٰسِرِينَ ﴿22﴾ فَإِنْ يَّصْبِرُواْ فَالنَّارُ مَثْوىٗ
لَّهُمْ وَإِنْ يَّسْتَعْتِبُواْ فَمَا هُم مِّنَ اَلْمُعْتَبِينَ ﴿23﴾ وَقَيَّضْنَا لَهُمْ قُرَنَآءَ
فَزَيَّنُواْ لَهُم مَّا بَيْنَ أَيْدِيهِمْ وَمَا خَلْفَهُمْ وَحَقَّ عَلَيْهِمُ اُلْقَوْلُ
فِيٓ أُمَمٍ قَدْ خَلَتْ مِن قَبْلِهِم مِّنَ اَلْجِنِّ وَالْإِنسِ إِنَّهُمْ كَانُواْ خَٰسِرِينَ ﴿24﴾
* وَقَالَ اَلَّذِينَ كَفَرُواْ لَا تَسْمَعُواْ لِهَٰذَا اَلْقُرْءَانِ وَالْغَوْاْ فِيهِ ربع
لَعَلَّكُمْ تَغْلِبُونَ ﴿25﴾ فَلَنُذِيقَنَّ اَلَّذِينَ كَفَرُواْ عَذَاباً شَدِيداً
وَلَنَجْزِيَنَّهُمُ أَسْوَأَ اَلَّذِي كَانُواْ يَعْمَلُونَ ﴿26﴾ ذَٰلِكَ جَزَآءُ أَعْدَآءِ اِللَّهِ اِلنَّارُ
لَهُمْ فِيهَا دَارُ اُلْخُلْدِ جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يَجْحَدُونَ ﴿27﴾
وَقَالَ اَلَّذِينَ كَفَرُواْ رَبَّنَآ أَرِنَا اَلَّذَيْنِ أَضَلَّٰنَا مِنَ اَلْجِنِّ
وَالْإِنسِ نَجْعَلْهُمَا تَحْتَ أَقْدَامِنَا لِيَكُونَا مِنَ اَلْأَسْفَلِينَ ﴿28﴾

20. Zasu fađa ga fatunsu donme kukayi shaida a kammu, sai sukace Allah ne ya furtar damu, wanda ya furtar da kowane abu, shine ya halicce ku marrar farko, izuwa gareshi ake komawa daku (mai iko a bisa ƙago samuwar kuda farko da rayaku bayan kun mutu, mai ikone bisa ya furtar da fatunkuda gaɓoɓinku).
21. Baku kasance kuna ɓuyaga miyagun al'amurra don kunnuwankuda idanunkuda fatakunku suyi muku mummunar shaida ba, (wato bakwa ɓuyaga buran aika aikin alfasha don kunnuwankuda idanunku suyi muku mummunar shaida ba, don baku bada gaskiya da tashin alƙiyama ba), kaidai kunyi zatone yayin ɓuyanku ccwa haƙiƙa Allah bai san yawanci daga abinda kuke ɓoyewa ba, (ɓuyan wawa kenan).
22. Wancanenku zatonku wanda kuka zatada Ubangijinku shine ya halakar daku, kuka zamo daga cikin taɓaɓɓu.
23. In sunyi haƙuri (a kan azaba), to wutace makomar su in suka nemi a yarda dasu, to su basu daga cikin ababan yarda.
24. Mun hukunta musu abokai na Shaiđanu suka ƙawata musu abinda yake gabansu (na daga sha'anin duniya, da bin sha'awaice-sha'awaice) suka ƙawata musu abinda yake bayansu (na daga lahira, saboda fađinsu ba tashi ba hisabi), magana ta azabata tabbata garesu, (Itace LALLAI ZAN CIKA JAHANNAMA, harya zuwa ƙarshen aya), a cikin jimlar al'ummatai data halaka daga gabansu na daga Aljanu da mutane, haƙiƙa su sun kasance taɓaɓɓu.

(KAFIRAI DA AIYUKANSU DA SAKAMAKONSU)

25. Wađanda suka kafirta suka fađa (yayin karatun Annabi Sallallahu alaihi wa sallama) kada kuyi sauraro ga wannan Alƙur'ani kuyi hargowa a cikinsa, wata kila kwa rinjayeshi (ya daina karatun alƙur'anin).
26. (Sai Ubangiji yace musu) "Lallai zamu đanđana wa wađanda suka kafirta azaba mai tsanani, lallai zamu saka musu da mafi munin abinda suka kasance suna aikatawa".
27. Wancanenka azaba matsananciya, sakamakon maƙiya Allah shine wuta, azabar dauwama na garesu a cikinta don sakamakon abinda suka kasance suna yin musu (na ayoyin alƙur'ani).
28. Wađanda suka kafirta (a cikin wuta) sukace, "Ya Ubangijinmu nuna mana mutum biyun nan da suka ɓatar damu na daga aljan da mutum, (Iblis da ƙabilu da suka sunnata kafirci da kisa) mu sanyasu ƙarƙashin dugaduganmu a cikin wuta donsu kasance daga mafi ƙasƙas đin maƙasƙasta, (wato mafiya tsananin yiwa azabadaga garemu).

إِنَّ الَّذِينَ قَالُواْ رَبُّنَا اللَّهُ ثُمَّ اَ۪سْتَقَامُواْ تَتَنَزَّلُ عَلَيْهِمُ
الْمَلَٰٓئِكَةُ أَلَّا تَخَافُواْ وَلَا تَحْزَنُواْ وَأَبْشِرُواْ بِالْجَنَّةِ
الَّتِي كُنتُمْ تُوعَدُونَ (29) نَحْنُ أَوْلِيَآؤُكُمْ فِي الْحَيَوٰةِ
الدُّنْيا وَفِي الْأٓخِرَةِ وَلَكُمْ فِيهَا مَا تَشْتَهِي أَنفُسُكُمْ
وَلَكُمْ فِيهَا مَا تَدَّعُونَ (30) نُزُلًا مِّنْ غَفُورٍ رَّحِيمٍ (31)
وَمَنْ أَحْسَنُ قَوْلًا مِّمَّن دَعَا إِلَى اللَّهِ وَعَمِلَ صَالِحًا وَقَالَ إِنَّنِي
مِنَ الْمُسْلِمِينَ (32) وَلَا تَسْتَوِي الْحَسَنَةُ وَلَا السَّيِّئَةُ اِدْفَعْ بِالَّتِي
هِيَ أَحْسَنُ فَإِذَا الَّذِي بَيْنَكَ وَبَيْنَهُ عَدَاوَةٌ كَأَنَّهُ وَلِيٌّ
حَمِيمٌ (33) وَمَا يُلَقَّىٰهَا إِلَّا الَّذِينَ صَبَرُواْ وَمَا يُلَقَّىٰهَا
إِلَّا ذُو حَظٍّ عَظِيمٍ (34) وَإِمَّا يَنزَغَنَّكَ مِنَ الشَّيْطَٰنِ نَزْغٌ
فَاسْتَعِذْ بِاللَّهِ إِنَّهُ هُوَ السَّمِيعُ الْعَلِيمُ (35) وَمِنْ ءَايَٰتِهِ
الَّيْلُ وَالنَّهَارُ وَالشَّمْسُ وَالْقَمَرُ لَا تَسْجُدُواْ لِلشَّمْسِ
وَلَا لِلْقَمَرِ وَاسْجُدُواْ لِلَّهِ الَّذِي خَلَقَهُنَّ إِن كُنتُمْ
إِيَّاهُ تَعْبُدُونَ (36) * فَإِنِ اسْتَكْبَرُواْ فَالَّذِينَ عِندَ رَبِّكَ سجدة ثمن
يُسَبِّحُونَ لَهُ بِالَّيْلِ وَالنَّهَارِ وَهُمْ لَا يَسْـَٔمُونَ (37)

(SHEHUNNAN DARIKAI NA SUFAYE)

29. Haƙiƙa waɗannan da sukace Allah shine Ubangijinmu, sannan sukayi daidai (a kan gwadaben gaskiya tauhidi da wninsa daga abinda ya wajaba a kansu), to Mala'iku zasu sauka a kansu (yayin mutuwa) cewa kada kuji tsoro (daga mutuwa wala abinda yake bayan mutuwa) kada kuyi baƙin ciki (a bisa abinda zaku bari a bayan ku a bisa ahalinkuda 'ya'yanku, Mune zamu maye muku gurabansu) munayi muku albishir da Aljanna, wacce kuka kasance anayi muku alwashi da ita.
30. Mune majiɓantarku a duniya, (muna kiyayeku a cikinta) da lahira (muna kasancewa a taredaku ,har ku shiga Aljanna) abinda kawukanku take marmari na gareta abinda kuke marmari na gareku.
31. Yasanya muku garar baƙi daga sarki mai gafara (shine Allah. Masu daidaito a kan gwadaben ubangiji sune kamar masu kira izuwa Allah, wato malaman Tauhidi kamar Lasha'ari da Maturidi da fukaha'u kamar Mala'ikuda makamantansu dasufaye kamar Junaidu da makamancinsa).
32. Babu mafi kyau a magana daga wanda yayi kira izuwa Allah yayi aiki na gari yace, " Haƙiƙa ni ina daga cikin Musulmi"[1].
33. Kyakykyawan aiki da mummuna bazasuyi daidai baka ije mummunan aiki da ta'ada wacce tafi kyau (wato ka ije fushi da haƙuri, ka ije wautada nutsuwa, ka ije ɓatawa da rangwame), saiga wanda tsakaninka dashi gabace, kaika ceshi masoyi ne mai tsananin kulawa dakai.
34. Ba wanda ake bashi wannan ta'ada sai waɗanda suka daure, ba wanda ake baiwa wannan ta'ada sai ma'abocin rabo mai girma.
35. Idan mai juyarwa na daga Shaiɗan ya juyar dakai ga buran kyakykyawar ta'ada) to ka nemi taimako da Allah, haƙiƙa Ubangiji shine maiji mai sani (yana jin maganar kowa yana da maganarsa).

(BA'ALIN MANA KAN ALLAH)

36. Yana daga ayoyin Ubangiji dare da wuni da rana da wata, kada kuyi sujada ga rana wala ga wata kuyi sujada ga Allah wanda ya halicce su, inkun kasance shi kaɗai kuke bautawa.
37. In sunyi girman kai ga yinsujada (ga Allah shi kaɗai), to Mala'ikun Allah waɗanda suke wajen Ubangijinka suna sallah gareshi dare da wuni alhali su basa ƙosawa.

1) Sawi yace: Wannan aya ta sauka ne cikin Ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wa sallama domin shine ya tara waɗancanenka sifofi saboda masu kira izuwa Allah kashi huɗu, masu kira izuwa Allah da tauhidi da harshe kamar Lash'ari da Maturidi da wanda ya bisu har izuwa ranar alƙiyama da masu kira izuwa Allah da hukunce-hukuncen shari'a kamar limana i guda huɗu da wanda yake bin dugaduganus, da masu kira dayayewar shamaki ga buran zuciyoyi saboda ganin hasken Ubangiji ta yaddazai zama turtur a fadar Allah, ba komai a zuciyarsa saishi, kamar Junaidu da masu kira izuwa Allah da sanarwa da bada farillai kamar masu kiran Sallah mafi girman masu kira izuwa Allah, Waliyai masu saduwa da halitta izuwa tafarkin Allah, suko samammune a kowane lokaci saidai cewa shi barnai saduwa dasu sai wanda Allah ya nufa. -Sawi-

وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنَّكَ تَرَى ٱلْأَرْضَ خَٰشِعَةً فَإِذَآ أَنزَلْنَا عَلَيْهَا
ٱلْمَآءَ ٱهْتَزَّتْ وَرَبَتْ إِنَّ ٱلَّذِےٓ أَحْيَاهَا لَمُحْيِ ٱلْمَوْتَىٰٓ إِنَّهُۥ عَلَىٰ
كُلِّ شَےْءٍ قَدِيرٌ ﴿38﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَلْحَدُونَ فِےٓ ءَايَٰتِنَا لَا يَخْفَوْنَ عَلَيْنَا
أَفَمَن يُلْقَىٰ فِے ٱلنَّارِ خَيْرٌ أَم مَّن يَأْتِےٓ ءَامِنًا يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ
ٱعْمَلُواْ مَا شِئْتُمُۥٓ إِنَّهُۥ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿39﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِٱلذِّكْرِ
لَمَّا جَآءَهُمْ وَإِنَّهُۥ لَكِتَٰبٌ عَزِيزٌ ﴿40﴾ لَّا يَأْتِيهِ ٱلْبَٰطِلُ مِنۢ بَيْنِ
يَدَيْهِ وَلَا مِنْ خَلْفِهِۦ تَنزِيلٌ مِّنْ حَكِيمٍ حَمِيدٍ ﴿41﴾ مَّا يُقَالُ لَكَ
إِلَّا مَا قَدْ قِيلَ لِلرُّسُلِ مِن قَبْلِكَ إِنَّ رَبَّكَ لَذُو مَغْفِرَةٍ
وَذُو عِقَابٍ أَلِيمٍ ﴿42﴾ وَلَوْ جَعَلْنَٰهُ قُرْءَانًا أَعْجَمِيًّا لَّقَالُواْ لَوْلَا
فُصِّلَتْ ءَايَٰتُهُۥٓ ءَا۬عْجَمِيٌّ وَعَرَبِيٌّ قُلْ هُوَ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ هُدًى
وَشِفَآءٌ وَٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ فِےٓ ءَاذَانِهِمْ وَقْرٌ وَهُوَ عَلَيْهِمْ عَمًى
أُوْلَٰٓئِكَ يُنَادَوْنَ مِن مَّكَانٍۢ بَعِيدٍ ﴿43﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَى
ٱلْكِتَٰبَ فَٱخْتُلِفَ فِيهِ وَلَوْلَا كَلِمَةٌ سَبَقَتْ مِن رَّبِّكَ
لَقُضِيَ بَيْنَهُمْ وَإِنَّهُمْ لَفِے شَكٍّ مِّنْهُ مُرِيبٍ ﴿44﴾ مَّنْ عَمِلَ صَٰلِحًا
فَلِنَفْسِهِۦ وَمَنْ أَسَآءَ فَعَلَيْهَا وَمَا رَبُّكَ بِظَلَّٰمٍ لِّلْعَبِيدِ ﴿45﴾

38. Yana daga cikin ayoyinsa cewa kai kana ganin ƙasa ƙeƙashashshiya, a cikinta batsiri idan muka saukar da ruwa a kanta saitayi motsi ta daɗu, haƙiƙa wanda ya rayata lallai mai raya matattu ne, haƙiƙa shi Ubangiji shi mai ikone bisa komai.

(BAN TSORO MAKANGARA A CIKIN ALƘUR'ANI)

39. Haƙiƙa waɗanda suke kangara da ayoyinmu na alƙur'ani bazasu ɓuyaba a garemu zamuyi musu sakamko, shin wandaka jefashi cikin wuta shine yafiko wanda zaizo yana amince ranar alƙiyama? (Wanda zaizo a amince yafi). Ku aikata abinda kuka ga dama Ubangiji mai ganin abinda kuke aikatawa ne.
40). Haƙiƙa waɗannan da suka kafirce da wannan alƙur'ani zamanin dayazo musu zanyi musu sakamako, haƙiƙa shi Alƙur'ani littafi ne mabuwayi.
41. ƙarya bata zuwa masa nan gaba gareshi wala daga bayansa (wato ba littafi da yake ƙaryatashi wala bayansa), shi saukarwa ne daga gwani abin godewa cikin al'amarinsa.
42. Ba a faɗa maka sai abinda aka faɗawa manzanni na gaban ka, haƙiƙa Ubangijinka mai gafara ne (ga muminai) mai uloibane mai raɗaɗi (ga kafirai).

(ALƘUR'ANI DA WAƊANDA SUKA KANGARA A CIKINSA)

43. Da mun sanyashi alƙur'ani na baibayi dasunce "Me ya sa ba a faiyace ayoyinsa ba? Yayakur'ani baubawa ga Annabi Balarabe? Ka faɗa "Shi alƙur'ani shiriya ne (daga bata) ga waɗanda suka bada gaskiya waraka ne (daga cutar jahilci da kuma dukkan cuta). Waɗanda basu bada gaskiya dashi ba ak-wai toshiya a cikinkunnuwansu shi makanta ne a kansu (bazasu fahince shi ba), wadancanenka (kamar) ana ki-ran sune daga guri manisanci, (da baza a ji kiran ba wato baza a fahimce shi basaboda zur-fin kafircinsu).
44. Haƙiƙa mun baiwa Annabi Musa Attaura aka sassaba a cikinsa (wadansu suka gasgata, wadansu suka ƙaryata kamar Alƙur'ani), ba don kalma data rigaya daga Ubangijinka ba (ta jirkinta sakamakon ranar alƙiyama) da an yi hukunci tsakaninsu (a duniya), haƙiƙa su masu ƙaryatawa dashi lallai suna cikin kokonto daga gareshi mai afkar dasu a cikin tuhuma.
45. Wanda yayi aiki nagari yayi ne don kansa, wanda yayi aiki mummuna ya aikata ne a kansa (ya cuci kansa) Ubangiji bai ka-sance mai zalinta ga bayinsa ba (saboda faɗinsa baya zalintar bayinsa misalin Kwayar ko-mayya).

حزب

* إِلَيْهِ يُرَدُّ عِلْمُ السَّاعَةِ وَمَا تَخْرُجُ مِن ثَمَرَٰتٍ مِّنْ أَكْمَامِهَا
وَمَا تَحْمِلُ مِنُ اُنثَىٰ وَلَا تَضَعُ إِلَّا بِعِلْمِهِۦ وَيَوْمَ يُنَادِيهِمُۥ
أَيْنَ شُرَكَآءِيَ قَالُوٓاْ ءَاذَنَّٰكَ مَا مِنَّا مِن شَهِيدٍ ﴿46﴾ وَضَلَّ
عَنْهُم مَّا كَانُواْ يَدْعُونَ مِن قَبْلُ وَظَنُّواْ مَا لَهُم مِّن مَّحِيصٍ ﴿47﴾
لَّا يَسْـَٔمُ الْإِنسَانُ مِن دُعَآءِ الْخَيْرِ وَإِن مَّسَّهُ الشَّرُّ فَيَـُٔوسٌ
قَنُوطٌ ﴿48﴾ وَلَئِنْ أَذَقْنَٰهُ رَحْمَةً مِّنَّا مِنۢ بَعْدِ ضَرَّآءَ مَسَّتْهُ
لَيَقُولَنَّ هَٰذَا لِي وَمَا أَظُنُّ السَّاعَةَ قَآئِمَةً وَلَئِن رُّجِعْتُ إِلَىٰ رَبِّيَ
إِنَّ لِي عِندَهُۥ لَلْحُسْنَىٰ فَلَنُنَبِّئَنَّ الَّذِينَ كَفَرُواْ بِمَا عَمِلُواْ
وَلَنُذِيقَنَّهُم مِّنْ عَذَابٍ غَلِيظٍ ﴿49﴾ وَإِذَا أَنْعَمْنَا عَلَى الْإِنسَانِ
أَعْرَضَ وَنَٰٓا بِجَانِبِهِۦ وَإِذَا مَسَّهُ الشَّرُّ فَذُو دُعَآءٍ عَرِيضٍ ﴿50﴾
قُلْ أَرَٰيْتُمْ إِن كَانَ مِنْ عِندِ اللَّهِ ثُمَّ كَفَرْتُم بِهِۦ مَنْ أَضَلُّ
مِمَّنْ هُوَ فِي شِقَاقٍ بَعِيدٍ ﴿51﴾ سَنُرِيهِمُۥ ءَايَٰتِنَا فِي الْآفَاقِ
وَفِي أَنفُسِهِمْ حَتَّىٰ يَتَبَيَّنَ لَهُمُۥ أَنَّهُ الْحَقُّ أَوَلَمْ يَكْفِ
بِرَبِّكَ أَنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ شَهِيدٌ ﴿52﴾ أَلَا إِنَّهُمْ فِي مِرْيَةٍ
مِّن لِّقَآءِ رَبِّهِمُۥ أَلَا إِنَّهُۥ بِكُلِّ شَيْءٍ مُّحِيطٌ ﴿53﴾

(SANIN LOKACIN ALƘIYAMA YANA GURIN UBANGIJI)

46. Izuwa ga Allah ne ake komo da ilimin yaushe alƙiyama ne zata tashi, babu 'ya'ya itatuwa da zasu fita daga kwasfanninta saida ilimin Ubangiji, (ba wanda yasan za tafitar da kwasfannin nata ko bazata fitar basai Allah) wata mata bazata haife ciki basaida ilimin Allah, (wato Allah ne yasan kwanu-kan cikin da kasancewarsa na-miji ko mace da lokacin haihu-wa da gurin haihuwa sai Allah, masu kashafi suna sani amma da kimsawar Allah, bokaye da masu taurari iliminsu na zato ne galibi a saninsu kuskure ne). A ranar da yake kiransu "Ina abo-kan tarayyar nawa?" Saisu ce, "Mun sanar dakai a yanzu babu wani mai shaidawa daga garemu cewa kana da wani abokin tarayya.
47. Abinda suke bautawa a duniya tun gaba (na daga gumaka) ya bace musu, sun kasance basu da wata makardada (nan da Ubangiji

(MUTUM DA DABI,ARSA)

48. Mutum ba yakosawa daga rokon alheri ,(yana rokon Ubangiji dukiya da lafiya da waninsu) in sherri ya sameshi (talauci da waninsa),to mai yawan debe haso ne (daga rahamar Ubangiji wannan da abinda yake bayansa sifar kafirai ce
49. Wallahi idan muka ɗanɗana masa rahama (wadatada lafiya) daga garemu, bayan tsanani da bala"i ...daya sameshi zai dinga cewa lalai wannan nawa ne (na,cancanceshi da aikina), bana "zaton alƙiyama zata tashi, wAllahi' in an koma dani izuwa Ubangijina haƙiƙa ina da Aljanna nan gareshi, lallai zamu ba wa waɗanda suka kafirta labarim da abinda suka aikata. Wailahi zamu ɗanɗana masu azabakak-kaura
50. In mukayi ni'ima ga mutum sai ya. bijire ga buran godiya sai yai nisa da gefansa yana mai takama, idan; sharri.) ya same shito ma,abocin addu,a ne mai fadi .

(SANIN ALLAH TAKAN DALILAI DA SANIN ALLAH TAKAN SHUHUDI)

51. Ka faɗa ku bani alƙur'ani ya ka-sance daga gun Allah (kamar da Annabi ya faɗa Sallallahu alaihi wa sallama) sannan kuka kafirta dashi ba ɗaya mafi ɓata daga wandashi yake cikin sabani mai nisa (ga barin gaskiya, wato ba mafi bata daga gareku).
52. Da sannu zamu nuna musu ayoyinmu a cikin sassan sam-mai da ƙassai (sune taurari da jirgin sama da jirgin ƙasa, da kumbo da talbijin da talfo da sauran irinsu da tsirrai da itatu-wa da manya-manyan waliyai da malamai masu aiki da sanin-su a kan istikama), kuma zamu nuna musu ayoyinmu a cikin kawukansu (na daga lallausan aiki da kyakkyawar hikima) har ya bayyana garesu cewa shi alƙur'ani Shine gaskiya (abin saukarwa daga Allah da tashin alƙiyama da hisabi da ukuba ayi musu ukuba bisa kafircewar da sukayi dashi da wanda yazo dashi). Shin Ubangiji bai isa cewa Shine mahalarci bisa komai ba, (wato bai ishesu a cikin gaskiyarka ba, cewa Ubangiji ba abinda yake fakuwa ga bu-ransa ba komai Rankantarsa).
53. To jama'a haƙiƙa su, suna cikin kokonto daga saduwa da Ubangijinsu, (saboda sunyi musun tashin aiRiyama ko dan rashin dandano a cikin ma'arifa) to jama'a haƙiƙa Ubangiji mai ke-wayewa ne da komai (ilimi da iko zaiyi musu sakamako da kafircinsu).

ثمن

42 سُورَةُ الشُّورَىٰ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ خَمْسُونَ ءَايَةً 50

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

* حمٓ عٓسٓقٓ كَذَٰلِكَ يُوحِيٓ إِلَيْكَ وَإِلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكَ ٱللَّهُ
ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ (1) لَهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلْأَرْضِ وَهُوَ ٱلْعَلِيُّ
ٱلْعَظِيمُ (2) يَكَادُ ٱلسَّمَٰوَٰتُ يَتَفَطَّرْنَ مِن فَوْقِهِنَّ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ
يُسَبِّحُونَ بِحَمْدِ رَبِّهِمْ وَيَسْتَغْفِرُونَ لِمَن فِي ٱلْأَرْضِ أَلَآ إِنَّ ٱللَّهَ
هُوَ ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ (3) وَٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ أَوْلِيَآءَ
ٱللَّهُ حَفِيظٌ عَلَيْهِمْ وَمَآ أَنتَ عَلَيْهِم بِوَكِيلٍ (4) وَكَذَٰلِكَ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ قُرْءَانًا
عَرَبِيًّا لِّتُنذِرَ أُمَّ ٱلْقُرَىٰ وَمَنْ حَوْلَهَا وَتُنذِرَ يَوْمَ ٱلْجَمْعِ لَا رَيْبَ فِيهِ
فَرِيقٌ فِي ٱلْجَنَّةِ وَفَرِيقٌ فِي ٱلسَّعِيرِ (5) وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ لَجَعَلَهُمُ أُمَّةً وَٰحِدَةً
وَلَٰكِن يُدْخِلُ مَن يَشَآءُ فِي رَحْمَتِهِۦ وَٱلظَّٰلِمُونَ مَا لَهُم مِّن وَلِيٍّ
وَلَا نَصِيرٍ (6) أَمِ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ أَوْلِيَآءَ فَٱللَّهُ هُوَ ٱلْوَلِيُّ وَهُوَ يُحْيِ ٱلْمَوْتَىٰ
وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ (7) وَمَا ٱخْتَلَفْتُمْ فِيهِ مِن شَيْءٍ فَحُكْمُهُۥٓ
إِلَى ٱللَّهِ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبِّي عَلَيْهِ تَوَكَّلْتُ وَإِلَيْهِ أُنِيبُ (8)

Wannan surata Shu-ra ce
A Makka aka saukar da ita Aya Hamsin ce (50)
Ina farawa dasunnan Ubangiji Mai jinkan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jin kan Muminai a lahira a keɓe

Ita Wannan Sura Ta kunshi Tauhidi Da Annabci Da Tabbatar Da Tashin alƙiyama Da Bincike Cikin Alƙur'ani Wanda Aka Saukar Ga Sayyidina Rassullullahi Sallallhu Alaihi Wasallama Kuma Da Kirari Da Alƙur'ani Da Dukkan Girma Da Kudurar Ubangiji Da Himinsa Da hikima Tasa Da Cewa Kuma Wannan Shari'a Ta Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama Tana Dacewa Da Shri'o'i Asalai Daga Shari' Waɗanda suka Rigayeshi A Cikin Asalai Ba Hanzari Ga Wanda ya Karfice Ba Hujja, Da Ban Tsoro Da Abinda Aka Tanada Ga Kafirai Da Abinda Aka Tanada Ga Muminai Da ambaton Ba'alin Ayoyinsa Da Bayanin Cewa Dukkan Aikace-Aikacensa Masu Dacewa Da Hikima Da Masalaha Tareda Bayanin Siffofin Mumunai Da Siffofin Waninsu Ya Tare Wannan Da Wahayi, Ya Cikatada Wahayi Da BayaninYadda Wahayi Ya Sadu Da Annbawa

(WANDA YA AIKO DA WANNAN ALƘU'RANI SHINE ALLAH)

1. Allahu a'alamu bi muradihi bi zalika kamar wancanenka (wahaitarwa) Ubangiji gwani mabuwayi
2. Yake aikowa gareka da waɗanda suke gabanka abinda ke sammai da ƙassaina Ubangiji ne (Mallaka da halitada bauta)shine maɗaukaki (kan halita tasa) mai girman sarautarsa
3. Sammai tana kusanta ta kyakykece daga burbushin kowace daya daga cikinsu (saboda girman Ubangiji) Mala'iku kuma suna tasbihi tareda gadiyar Ubangijinsu suna neman gafara ga waɗanda suke cikin ƙasa (na muminai) mai jinƙai (dasu) Waɗanda suka riki wanin Allah gumaka Allah mai kewa ne a kansu kai ba wakili ne a kansu (da zaka tilashe su bada gaskiya) ba

(HMIRORI NA MUSULUNCI) GAMAWAR KIRAN ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAMA GA DUKKAN SASSAN DUNIYA HAR IZUWA TASHIN ALƘIYAMA)

5. Irin wancanenka aikowa muka aiko izuwa gareka kur'ani Bala-rabe domin ka tsiratar da muta-nen Makka da sauran mutane, (wato mutanen duniyagaba ɗaya hatta mutanen sama), kuma ka tsorar dasu tsaiwar aifayama ba kokonto a cikinsa wata lomgiyar tasu tana cikin al-janna, wata kungiyar tana cikin wuta.
6. Da Allah yaga dama da saiya mai dasu al'umma guda ɗaya (kan addini ɗaya, Musulunci ko kafirci) saidai yana shigar da v/andayaga dama a cikin raha-marsa, azzalumai kuwa (wato kafirai) basu da majibinci wala mai taimako (dazai ije musu azabar Ubangiji).
7. Bari! Sudai sun riki iyayen giji ba Allah ba (wato sun riki gu-maka, akwai wadansu mutane dasuke saukar da irin waɗannan ayoyi a kan Annabawa da wa-liyai, to waɗannan mutane 'yan katsiro ne, masu bidi'a ne, ba wani malamin tafsiri daya taɓa sakin waɗannan ayoyi a kan Anbiya'u da Auliya'u illa 'yan wahabiya. Allah ya shirye mu baki ɗaya) to Allah Shine matai-makin muminai, Shine mai raya (matattu), shi mai ikone bisa kowane abu.
8. Duk abinda kukayi sabani a cikinsa (tareda muminai na daga wani abu na Addini), to hukun-cinsa abin mayarwa ne izuwa Allah, ranar alƙiyama za a fayy-ace hukunci tsakanin ku, cene (dasu), "wancanenku Allah ke nan Ubangijina, a gareshi na do-gara, izuwa gareshi nake ko- mawa".

فَاطِرُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ جَعَلَ لَكُم مِّنْ أَنفُسِكُمْ أَزْوَٰجًا
وَمِنَ ٱلْأَنْعَٰمِ أَزْوَٰجًا يَذْرَؤُكُمْ فِيهِ لَيْسَ كَمِثْلِهِۦ شَىْءٌ
وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْبَصِيرُ ﴿٩﴾ لَهُۥ مَقَالِيدُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ
يَبْسُطُ ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقْدِرُ إِنَّهُۥ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿١٠﴾
۞ شَرَعَ لَكُم مِّنَ ٱلدِّينِ مَا وَصَّىٰ بِهِۦ نُوحًا وَٱلَّذِىٓ
أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ وَمَا وَصَّيْنَا بِهِۦٓ إِبْرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ وَعِيسَىٰٓ
أَنْ أَقِيمُوا۟ ٱلدِّينَ وَلَا تَتَفَرَّقُوا۟ فِيهِ كَبُرَ عَلَى ٱلْمُشْرِكِينَ
مَا تَدْعُوهُمْ إِلَيْهِ ٱللَّهُ يَجْتَبِىٓ إِلَيْهِ مَن يَشَآءُ وَيَهْدِىٓ إِلَيْهِ مَن
يُنِيبُ ﴿١١﴾ وَمَا تَفَرَّقُوٓا۟ إِلَّا مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلْعِلْمُ بَغْيًۢا بَيْنَهُمْ
وَلَوْلَا كَلِمَةٌ سَبَقَتْ مِن رَّبِّكَ إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى لَّقُضِىَ بَيْنَهُمْ
وَإِنَّ ٱلَّذِينَ أُورِثُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ مِنۢ بَعْدِهِمْ لَفِى شَكٍّ مِّنْهُ مُرِيبٍ ﴿١٢﴾
فَلِذَٰلِكَ فَٱدْعُ وَٱسْتَقِمْ كَمَآ أُمِرْتَ وَلَا تَتَّبِعْ أَهْوَآءَهُمْ وَقُلْ
ءَامَنتُ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ مِن كِتَٰبٍ وَأُمِرْتُ لِأَعْدِلَ بَيْنَكُمُ
ٱللَّهُ رَبُّنَا وَرَبُّكُمْ لَنَآ أَعْمَٰلُنَا وَلَكُمْ أَعْمَٰلُكُمْ لَا حُجَّةَ
بَيْنَنَا وَبَيْنَكُمُ ٱللَّهُ يَجْمَعُ بَيْنَنَا وَإِلَيْهِ ٱلْمَصِيرُ ﴿١٣﴾

رُبع

9. "Mai kagen sammai da ƙassai yasanya muku mataye daga cikin kawukanku (daya halicci Hau-wa'u daga hakarkarin Adamu Alaihimassalamu), yasanya muku daga dabbobi maramara, mazaje da mataye, ba wani abu kamar Ubangiji shi mai ji ne (ga abinda ake faɗa) mai gani (ga abinda ake aikatawa).
10. "Mabudan sammai da ƙassai (wato mabudan ta.skokin rwa da tsiri da waninsu) yana gareshi, yana yalwata arziki ga wan-dayaga dama (don gwaciawa) yana kuntatawa *ga wanda ya* gu dama (don gwadawa), haƙiƙa shi masani.ne da komai".

(HIKIMAR AIKE NA MAi^ZON ALLAH DA MANUFARTA)

11. Ya shardanta maku. abin du yayiwa Annabi Nuhu wasiya dashi (Shine Addini, Shine farkon Annabawa na shari'a) da abm da muka aiko izuwa gareka da abinda muka aiko Annabi Ibra-himu dashi da Annabi Isa du Annabi Musa, cewa ku tsaida Addini kem, kada kuyi daban-daban (a cikinsa Shine wanda aka aiko izuwa Annabi Salialla-hu alaihi wa sallama Shine tau-hidi), abinda kake kiran mushu -rikai izuwa gareshi (na tauhidi), ya girma garesu, Aliah ne yake zabar wanda yaga dama izuwa gareshi (wato izu.wa tauhulins?yana shiriyar wanda yakoma izuwa gareshi (da a'a).
12. Ma'abota addinai basuyida-ban-daban ba (wato wani ya kadaita wani ya kafirta) ba, sai bayan ilimi (na tauhidi) ya zamusu don zalinci a tsakaninsu ba don kalma da rinjaye daga Ubangijinka ta gabata ba izuwa ajali abin anbato (Shine ranar alƙiyama) da an yi hukunci tsakaninsu (da azabtar kafirai a duniya) haƙiƙa waɗanda aka gada musu littafi bayansu (sune Yahudu da Nasara) suna cikin kokonto daga Annabi (Sallalla-hu alaihi wa sallama), mai af-karwa a cikin tuhuma.
13. To kayi ta kira izuwa wance-nenka (tauhidi) kayi daidai (a kan kiran bisa abinda aka umarce ka a kan kiran kada kabi soye-soyen sukatansu (a cikin barin tauhidi), Cene "Na bada gaskiyaga abinda Allah ya saukar na littafi an umarce ni in yi hukunci tsakaninku cikin adalci, Allah Shine Ubangijinku ayyukanmu na garemu ayyu-kanku na gareku zai sakawa kowaabinda ya aikata, ba husuma tsakaninmu daku ,(wan-nan tun gaban ba a umarce shi dayaRi bane). Allah zai tara tsakaninmu ranar lahira (don hukunci), izuwa gareshi zamu koma.

وَالذِينَ يُحَآجُّونَ فِے اِ۬للَّهِ مِنۢ بَعْدِ مَا اَ۟سْتُجِيبَ لَهُۥ
حُجَّتُهُمْ دَاحِضَةٌ عِندَ رَبِّهِمْ وَعَلَيْهِمْ غَضَبٞ وَلَهُمْ
عَذَابٞ شَدِيدٌ ﴿14﴾ اُ۬للَّهُ اُ۬لذِے أَنزَلَ اَ۬لْكِتَٰبَ بِالْحَقِّ وَالْمِيزَانَ
وَمَا يُدْرِيكَ لَعَلَّ اَ۬لسَّاعَةَ قَرِيبٞ ﴿15﴾ يَسْتَعْجِلُ بِهَا
اُ۬لذِينَ لَا يُومِنُونَ بِهَا وَالذِينَ ءَامَنُواْ مُشْفِقُونَ مِنْهَا
وَيَعْلَمُونَ أَنَّهَا اَ۬لْحَقُّ أَلَآ إِنَّ اَ۬لذِينَ يُمَارُونَ فِے اِ۬لسَّاعَةِ
لَفِے ضَلَٰلِۢ بَعِيدٍ ﴿16﴾ اُ۬للَّهُ لَطِيفُۢ بِعِبَادِهِۦ يَرْزُقُ مَنْ يَّشَآءُ
وَهُوَ اَ۬لْقَوِيُّ اُ۬لْعَزِيزُ ﴿17﴾ مَن كَانَ يُرِيدُ حَرْثَ اَ۬لَاخِرَةِ
نَزِدْ لَهُۥ فِے حَرْثِهِۦ وَمَن كَانَ يُرِيدُ حَرْثَ اَ۬لدُّنْيَا نُوتِهِۦ مِنْهَا
وَمَا لَهُۥ فِے اِ۬لَاخِرَةِ مِن نَّصِيبٍ ﴿18﴾ * أَمْ لَهُمْ شُرَكَٰٓؤُاْ شَرَعُواْ لَهُم ثمن
مِّنَ اَ۬لدِّينِ مَا لَمْ يَأْذَنۢ بِهِ اِ۬للَّهُ وَلَوْلَا كَلِمَةُ اُ۬لْفَصْلِ لَقُضِيَ
بَيْنَهُمْ وَإِنَّ اَ۬لظَّٰلِمِينَ لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٞ ﴿19﴾ تَرَى اَ۬لظَّٰلِمِينَ
مُشْفِقِينَ مِمَّا كَسَبُواْ وَهُوَ وَاقِعُۢ بِهِمْ وَالذِينَ
ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ اُ۬لصَّٰلِحَٰتِ فِے رَوْضَاتِ اِ۬لْجَنَّاتِ
لَهُم مَّا يَشَآءُونَ عِندَ رَبِّهِمْ ذَٰلِكَ هُوَ اَ۬لْفَضْلُ اُ۬لْكَبِيرُ ﴿20﴾

14. Wađannan dasuke jayayya cikin sha'anin Ubangiji (suke jayayya da Annabi Sallallahu alaihi wa sallama) bayan an amsa masa da imani, saboda bayyanarsa da mu'ujiza, (sune Yahudu), Huj-jarsu zamammiyace nan ga Ubangijinsu, fushi na garesu, azaba mai tsanani ta tabbata garesu.
15. Allah ne sarkin daya saukar da Alƙur'ani da gaskiya da adalci, Menene yasanar dakai wata kila Alƙiyama a kusa take?
16. Wađanda basu bada gaskiya da ita basuna gaggauto da ita. amma wađanda suka bada gaskiya da ita masu tsoro ne gareta, sunsan cewa ita alƙiyama gaskiyace. Na'am, wađannan dasuke jayayya cikin sa'a ta Alƙiyama lallai suna cikin bata manisanci (ga buran gaskiya).
17. Allah mai tausayawa ne ga bay-insa (nagarinsu da lalataccensu) yana azurta wanda yaga dama daga (cikinsu) shi mai karfi ne (kan abinda yake nufi) mai rin-jaye ne (kan al'amarinsa)

(MASU AIKI DA ILIMI DA SAKAMAKONSU)

18. Wanda yake nifin sakamakon lahira da aikinsa; za Kara masa a cikin sakamakonsa (da ninnin-kawa hasana đaya izuwa goma ko fiye) wanda yake nutin sa-kan'iakon duniya, nia ba 'si'ii gwargwadon rabonsa (bada mnninkawa), bashi da rabo a ranar lahira.
19. To bari! 'Shin suna da sharikaine đa suka shor'anta na da,ga ad" dini na banza, abinda Aliah bai yi izini dashi ba (kamar shirka da musum Alƙiyama? Ba don kalmar rabe hukunci ba (da cewa sakamako sai ranar iahi-ra), da an yi hukimci tsakariinsu da tsakanin muminai- (dayi musu -azaba a duniya); Siakifca kafirai azaba mai rađađi ta tabba-ta a garesu.
20. Kana gurin kafirai ranar alƙiyama suna masu tsoratada abin.da suka aikata (a di.iniya na daga miyagun ayyuka ayi musu sakamako a kanta?) Sh?. sakam-akon nan a kanta mai afkuwa ne a kansu (ranar alƙiyama) bada kokonto ba. Wađanda suka bada gaskiya sukayi ayynkka na-gargaru suna cikin dausayan aljannatai, abinda suke marmari;yana garesu nan ga Ubangijinsu wancanenka Shine falala;mai girma.

ذَٰلِكَ ٱلَّذِي يُبَشِّرُ ٱللَّهُ عِبَادَهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِۖ
قُل لَّآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ أَجْرًا إِلَّا ٱلْمَوَدَّةَ فِي ٱلْقُرْبَىٰۖ وَمَن يَقْتَرِفْ حَسَنَةً
نَّزِدْ لَهُۥ فِيهَا حُسْنًاۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ شَكُورٌ ﴿21﴾ أَمْ يَقُولُونَ
ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًاۖ فَإِن يَشَإِ ٱللَّهُ يَخْتِمْ عَلَىٰ قَلْبِكَۖ
وَيَمْحُ ٱللَّهُ ٱلْبَٰطِلَ وَيُحِقُّ ٱلْحَقَّ بِكَلِمَٰتِهِۦٓۖ إِنَّهُۥ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ
ٱلصُّدُورِ ﴿22﴾ وَهُوَ ٱلَّذِي يَقْبَلُ ٱلتَّوْبَةَ عَنْ عِبَادِهِۦ وَيَعْفُواْ عَنِ
ٱلسَّيِّـَٔاتِ وَيَعْلَمُ مَا يَفْعَلُونَ ﴿23﴾ وَيَسْتَجِيبُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ
ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَيَزِيدُهُم مِّن فَضْلِهِۦۚ وَٱلْكَٰفِرُونَ لَهُمْ عَذَابٌ شَدِيدٌ ﴿24﴾
وَلَوْ بَسَطَ ٱللَّهُ ٱلرِّزْقَ لِعِبَادِهِۦ لَبَغَوْاْ فِي ٱلْأَرْضِ
وَلَٰكِن يُنَزِّلُ بِقَدَرٍ مَّا يَشَآءُۚ إِنَّهُۥ بِعِبَادِهِۦ خَبِيرٌۢ بَصِيرٌ ﴿25﴾
وَهُوَ ٱلَّذِي يُنَزِّلُ ٱلْغَيْثَ مِنۢ بَعْدِ مَا قَنَطُواْ وَيَنشُرُ رَحْمَتَهُۥۚ وَهُوَ ٱلْوَلِيُّ
ٱلْحَمِيدُ ﴿26﴾ وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦ خَلْقُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَثَّ فِيهِمَا مِن دَآبَّةٍۚ
وَهُوَ عَلَىٰ جَمْعِهِمْ إِذَا يَشَآءُ قَدِيرٌ ﴿27﴾ وَمَآ أَصَٰبَكُم مِّن مُّصِيبَةٍ
بِمَا كَسَبَتْ أَيْدِيكُمْ وَيَعْفُواْ عَن كَثِيرٍ ﴿28﴾ وَمَآ أَنتُم بِمُعْجِزِينَ
فِي ٱلْأَرْضِۖ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِن وَلِيٍّ وَلَا نَصِيرٍ ﴿29﴾

(FALALAR 'YA YAN DAKINSA SALLALLAHU AI.AIHI WA SALLAMA WANDASHIWAGABANNIN DARIK0KIN SUFAYE SUNA DAGA CIKINSU KAMAR KUDUBAI GUDA HUDU' SHEHU ABDUI.KADIR .JILANIDA SHEHU AHMADURRUFA I DA SHEHU IBRAHIMUDDASURI DA SHEHU AHMADUI/BADAWI ALLAH YA KARA MUSIf YARDA rKITAIWI.r AHTSHINE 1V1 A SJOGA KA SHAIHANA N JARIkA. MUN GODE WA ALLAHI)

21. Wanconenka Shine abm da A1-lah alhi:,hir dashi ga bayinsa waɗanda suka bada gaskiyakuma sukayi ayvukka nagarga ru, Cene ni"bana tambayar ku lada a kan ida aike sai kauna a cikin zumuncina" (wato kaunar Ahlibaiti Sallallahu alaihi wasallama, Ance Ansaru, Ance Kuraishu amma tawailin farko yafi dacewa saboda hadisin da aka nswaito daga Zaidu dan Arkania ga Annabi Sallallahu alaibi wa sallania cewa shi yace, " haƙiƙa ni mai bdrin mafifita guda biyu a cikin ku ne-, littafin Allah da "ya'yars dakina aka". ce da Zaidu dan Arkama "Su waye 'yan dakinsa?" Yace Alu Aliyu, Aiu Akilin da Alu Ja'afarin da Alu A.bbasin" -Sawi yace, "kaunar Ahlul baiti akwai arziki da shugabanci a cikinta duniya da lahira mutum ana tara shi da wanda yake kauna") wanda ya aikata da'a zamu kara masa sa-kamakonta) (mu nunnuka masa saka makonta) ha^ika Ubangyi mai gafara ne (ga zunubai) mai godiya ne (ga kankanen aiki ya ninninka sakamakonsa).
22. Bari! suna cewa "Ya kagi karya ne izuwa Allah (da dangana shariki ga Allah"), in Ubangiji yaga dama saiya saka dauriya a kan zuciyarka (da hakuri a kan cutarsu, ta wannan magana da waninita.yakuwa aikata din),ubangiji zai shafe karya (wacce suka tadeta) zai saukar da gaskiya da kalmominsa (a bisa Annabinsa) to haƙiƙa Ubangiji masanine da haluluwan zukatan bayinsa
23. Shine yake harbar tubadaga bayinsa yake rangwame ga buran miyagun ayyuka,yake sanin abinda suke aikatawa
24. Yana amsawa waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru., yana amsa musu (abinda suka roke shi) yana kara musu daga falalarsa, kafirai kuwa azaba mai tsanani ta tabbata garesu.

(WANI ABU DAGA, MANA KIN HikiMAR UBANGIJI DA iKONSA)

25. DA Ubangiji ya shimfide arziki *ga* bayinsa (dukkansu) dasun yi zalinci a bayan ƙasa, saidai yana saukar da gwargwado abinda yake so, haƙiƙa Ubangiji masanine (da boyayyen halin bayinsa), mai ganine (dasu).
26. Shine wanda yake saukar da ruwa bayan sun debe haso (daga saukarsa), yake daidaita raha-marsa (wato ruwa), Shine mai kyautawa (ga inummai), abin godewa (nan garesu).
27. Yana daga cikin ayoyinsa haiit-^ar sammai da ƙassaida halittar abinda Ubangiji ya yada a bayan ƙasa na daga dabba mai mot-si a kan ƙasa na inntum da wa-ninsa, shi mai ikone bisa tara su in yaga dama.
28. Duk abinda ya same ku na ma-sifa, saboda abinda hannun mu ta gabatar ne (inu niuka saya aka sayar mana) yana rang-wame bisa yavvaici, (bazai sak-amako kan ta ba. to shi Ubangiji ta'ala yafi gaban ya sake saka-myko a lahira, amma wanin muznubai duk abinda ya samesu a duniya saboda daukaka da-rajojin sune a lahira),
29. Ku ba masu tserewa Allah bane a gudu a cikin ƙasa bare ku tsere masa, bakuda wani mataimaki ba Allah ba

وَمِنْ ءَايَٰتِهِ الْجَوَارِ فِي الْبَحْرِ كَالْأَعْلَٰمِ إِن يَشَأْ يُسْكِنِ الرِّيَٰحَ
فَيَظْلَلْنَ رَوَاكِدَ عَلَىٰ ظَهْرِهِۦٓ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٖ لِّكُلِّ صَبَّارٖ شَكُورٍ ﴿30﴾
ربع * أَوْ يُوبِقْهُنَّ بِمَا كَسَبُواْ وَيَعْفُ عَن كَثِيرٖ ﴿31﴾ وَيَعْلَمَ الَّذِينَ
يُجَٰدِلُونَ فِي ءَايَٰتِنَا مَا لَهُم مِّن مَّحِيصٖ ﴿32﴾ فَمَا أُوتِيتُم مِّن شَيْءٖ
فَمَتَٰعُ الْحَيَوٰةِ الدُّنْيَا وَمَا عِندَ اللَّهِ خَيْرٞ وَأَبْقَىٰ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَلَىٰ رَبِّهِمْ
يَتَوَكَّلُونَ ﴿33﴾ وَالَّذِينَ يَجْتَنِبُونَ كَبَٰٓئِرَ الْإِثْمِ وَالْفَوَٰحِشَ
وَإِذَا مَا غَضِبُواْ هُمْ يَغْفِرُونَ ﴿34﴾ وَالَّذِينَ اسْتَجَابُواْ لِرَبِّهِمْ
وَأَقَامُواْ الصَّلَوٰةَ وَأَمْرُهُمْ شُورَىٰ بَيْنَهُمْ وَمِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ يُنفِقُونَ ﴿35﴾
وَالَّذِينَ إِذَا أَصَابَهُمُ الْبَغْيُ هُمْ يَنتَصِرُونَ ﴿36﴾ وَجَزَٰٓؤُاْ سَيِّئَةٖ سَيِّئَةٞ
مِّثْلُهَا فَمَنْ عَفَا وَأَصْلَحَ فَأَجْرُهُۥ عَلَى اللَّهِ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ الظَّٰلِمِينَ ﴿37﴾
وَلَمَنِ انتَصَرَ بَعْدَ ظُلْمِهِۦ فَأُوْلَٰٓئِكَ مَا عَلَيْهِم مِّن سَبِيلٍ ﴿38﴾ إِنَّمَا السَّبِيلُ
عَلَى الَّذِينَ يَظْلِمُونَ النَّاسَ وَيَبْغُونَ فِي الْأَرْضِ بِغَيْرِ الْحَقِّ
أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٞ ﴿39﴾ * وَلَمَن صَبَرَ وَغَفَرَ إِنَّ ذَٰلِكَ لَمِنْ ثمن
عَزْمِ الْأُمُورِ ﴿40﴾ وَمَن يُضْلِلِ اللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن وَلِيّٖ مِّنۢ بَعْدِهِۦ
وَتَرَى الظَّٰلِمِينَ لَمَّا رَأَوُاْ الْعَذَابَ يَقُولُونَ هَلْ إِلَىٰ مَرَدّٖ مِّن سَبِيلٖ ﴿41﴾

30. Jiraga kamar duwarwatsu man-ya-manya a cikin kogi yana daga cikin ayoyin Ubangiji masu nuna ayarsa, in yaga dama saiya nutsar da ita sai ji-raga suyibanbaro a kan doron kogi bazasuyimotsi ba, haƙiƙa akwai ayoyi a cikin wan-canenka ga dukkan mai dauriya mai godiyaga Ubangiji.

31. Ko ya halakar dasu (ya nutsar dasu da tasowar iska mai tsana-ni saboda abinda suka aikata na daga zunubai), yana rangwame ga yawaici (na zunubai bazai nutsar da mutanen nata ba).

32. Yasan waɗanda suke jayayya cikin ayoyinsa basu da makardada daga azabar Ubangiji.

33. To duka abinda aka baku ku muminai da waninsu na koMenene na tarkacen duniya to wan-nan anfanin rayawar duniya ne kawai (a ji daɗi shiya gushe), abinda yake gurin Allah (na sakamako) Shine yafi wanzu-wa ga waɗanda suka bada gaskiya suke dogaro bisa Ubangijinsu.

(WANI ABU DAGA SIFOFIN MUMINAI)

34. Waɗannan dasuke nisanta ga manya-manyan zunnubai da aiyukan alfasha (masu wajabta haddodi), idan kuma sukayi fu-shi, su suna gafara (ga wanda ya fusatar dasu).

35. Kuma waɗanda suke amsawa Ubangiji (abinda ya kira na tau-hidi da ibada) kuma suka dau-wama kan sallah (da hakkokinta na zahiri dana badini) kuma al'amarinsu (wanda yake bayya-na garesu), shawara a tsakanin-su, (basa gaggawa a cikinsa sai sun yi shawara) kuma suna ciyarwa (a cikin da'ar Allah) daga abinda muka azurta musu.

36. Sune waɗanda idan zalinci ya samesu sukan yi sakayya (daga wanda ya zalince su), da abinda yayi daidai da zalinci da akayi musu.

37. (Kamar yadda Ubangiji yace) sakamakon mummuna, mum-muna daidai da ita, (don haka wanda yace, "Allah yakunya-tar da kai"), to wanda yayi rangwame (ga wanda ya zalince shi) ya kyauta (soyayya tsaka-ninsa da tsakanin wanda aka yiwa rangwame) to sakamakon-sa yana ga Allah, haƙiƙa Ubangiji bayason masu fara zalinci, (UKubarsa saitashiryu a kan-su).

38. Lallai wanda yayi sakayya bay-an an zalince shi, to wadancanenka babu hanya (ta riƙo da azaba a garesu).

39. Dahir dai hanya ta riRo da azabata tabbata a kan waɗanda ske za-lintar mutane, sukc zalinci da saɓo bada gaskiya ba, wadan-canenka azaba mai raɗaɗi ta tab-bata a garesu.

40. Lallai kuma wanda ya daure (bai yi sakayya ba) yayi gafara, haƙiƙa wannan (dauriyan nan da gafara nan),yana daga cikin al'amura (ababan nema a sha-ri'a).

(WAƊANNAN KUMA. SUNE KAFIRAI)

41. Wanda Allah ya ɓatar dashi to bashi da majibincin shiriya bay-ansa, kana ganin azzalumai (wato kafirai) yayin da suka ga azabasuna cewa "Yalla akwai damar komawa (izuwa du-mya?").

1) Sawı yace, an shardanta ita gafara ta zama ba mai Batawa da muruwwa ba,kuma fushin ya zama ba wajibi ba, in wajibi ne to fushi abin nema ne tamfar da idan aka keta alfarmar Ubangiji, to wajibi a sannan ne yin fushi ba rangwame ba, a nan ne Imamunu Shafi'i yake cewa, "wanda aka fusatar dashi bai fi-shi ba to shi jaki ne". -Sawi -

وَتَرَىٰهُمْ يُعْرَضُونَ عَلَيْهَا خَٰشِعِينَ مِنَ الذُّلِّ يَنظُرُونَ
مِن طَرْفٍ خَفِيٍّ وَقَالَ الَّذِينَ ءَامَنُوا إِنَّ الْخَٰسِرِينَ الَّذِينَ
خَسِرُوا أَنفُسَهُمْ وَأَهْلِيهِمْ يَوْمَ الْقِيَٰمَةِ أَلَا إِنَّ الظَّٰلِمِينَ
فِي عَذَابٍ مُّقِيمٍ (42) وَمَا كَانَ لَهُم مِّنْ أَوْلِيَآءَ يَنصُرُونَهُم
مِّن دُونِ اللَّهِ وَمَن يُضْلِلِ اللَّهُ فَمَا لَهُ مِن سَبِيلٍ (43)
اِسْتَجِيبُوا لِرَبِّكُم مِّن قَبْلِ أَن يَأْتِيَ يَوْمٌ لَّا مَرَدَّ لَهُ مِنَ اللَّهِ
مَا لَكُم مِّن مَّلْجَإٍ يَوْمَئِذٍ وَمَا لَكُم مِّن نَّكِيرٍ (44) فَإِنْ أَعْرَضُوا
فَمَا أَرْسَلْنَٰكَ عَلَيْهِمْ حَفِيظًا إِنْ عَلَيْكَ إِلَّا الْبَلَٰغُ
وَإِنَّا إِذَا أَذَقْنَا الْإِنسَٰنَ مِنَّا رَحْمَةً فَرِحَ بِهَا وَإِن تُصِبْهُمْ
سَيِّئَةٌ بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ فَإِنَّ الْإِنسَٰنَ كَفُورٌ (45)
لِّلَّهِ مُلْكُ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ يَخْلُقُ مَا يَشَآءُ يَهَبُ لِمَن يَشَآءُ إِنَٰثًا
وَيَهَبُ لِمَن يَشَآءُ الذُّكُورَ (46) أَوْ يُزَوِّجُهُمْ ذُكْرَانًا وَإِنَٰثًا
وَيَجْعَلُ مَن يَشَآءُ عَقِيمًا إِنَّهُ عَلِيمٌ قَدِيرٌ (47) * وَمَا كَانَ لِبَشَرٍ ربع
أَن يُكَلِّمَهُ اللَّهُ إِلَّا وَحْيًا أَوْ مِن وَرَآءِ حِجَابٍ أَوْ يُرْسِلَ
رَسُولًا فَيُوحِيَ بِإِذْنِهِ مَا يَشَآءُ إِنَّهُ عَلِيٌّ حَكِيمٌ (48)

42. Kana ganinsu ana bijirar dasu a kan wuta suna firgitattu saboda wulakanci, suna duba izuwa wutan nan daga idanu mai rau-nin duba, (wato suna satar kal-lo), waɗanda suka bada gaskiya sukace, " Haƙiƙanin taɓaɓɓu sune waɗanda suka taɓar da kansu da iyalinsu ranar alƙiyama, (da dauwamar dasu a wuta, da ra-shin saduwarsu izuwa Hu-rul'ainu, wacce aka tanadar musu a cikin aljanna dasun bada gaskiya), Na'am. haƙiƙa kafirai suna cikin azaba madauwa-miya (inji Ubangiji).
43. Basu da majibintada zasu tai-make su ba Allah be, wanda Allah ya ɓatar dashi, (ga buran gaskiya a duniya), bashi da wata hanya (izuwa aljanna a la-hira).

(AL'AMARI DUKA NA ALLAH NE)

44. Ku anntsawa Ubangijinku (da tauhidi da ibada) tun gaban rana batazo ba, wacce ta juyarwa gareta, (Itace alƙiyama), bakuda wata mafaka (wacce zaku fake gareta a wannan rana) bakuda damar yin musun zunu-ban ku.
45. To in sun bijire ga buran ansaw-ar, to bamu aiko ka kana mai kiyayewa a kansu (da aiyukan-su) ba, (ma'ana bamu aiko donka halicci shiriya a cikin zuka-tansu ba, ka sanya ayyukansu mai dacewa ga abinda muka nema daga garesu) babu wani abu daga gareka illa iyad da aike, (wannan ya tabbata gaban umarni dayaƙi), haƙiƙa in muka ɗanɗanawa mutane rahama daga garemu (kamar wadatada la-fiya) sai sukan yi murna da ita, idan bala'i ya samesu saboda abinda hannuwansu ta gabatar, to mutum mai butulcewa ne (ga ni'imar Allah).
46. Mulkin sammai da ƙassaina Allah ne yana halittar abinda yaga dama, yana baiwa wanda yaga dania daga 'ya'ya mata, yana baiwa wanda yaga dama ma-zaje.
47. Ko kuma yasanya su ma zaje da mataye, yana mai da ^andayaga dama bakarara, (bazai haihu badaza a haifa masa ba), hafdKa shi Ubangiji masanine (da abinda yake halitta) mai ikone (bisa abinda yaga dama).

(YADDA UBANGIJI YAKE SADUWADA MANZANNINSA)

48. Bazai yiwu ga muturo Allah yayyi zance dashi basai ko Allah yayi masa wahayi (a cikin mafarki) ko a bayan shamaki (Shine ko yajiyar dashi zan-censa, a halin baya ganinsa) [1] ko ya aiko manzo Mala'ika (ka-mar Jibrilu), to shi manzon nan ya c.adar da wannan Annabi da izinin Allah, haƙiƙa Ubangiji madaukaki ne (cikin aikinsa).

1) Haƙiƙa Ilhami yana afkuwa ga wanin Anna-bawa kamar waliyai, amma Ilhamin walıyai bai kai ya na Annabawa karfi ba, domin An-nabawa ma'asumai ne, waliyai kuwa pnahfu-zai ne, wato ababan kiyayewa ne, wato basu kai ga ISMA ba. -Sawi-

وَكَذَٰلِكَ أَوْحَيْنَا إِلَيْكَ رُوحًا مِّنْ أَمْرِنَا مَا كُنتَ تَدْرِي مَا الْكِتَٰبُ
وَلَا الْإِيمَٰنُ وَلَٰكِن جَعَلْنَٰهُ نُورًا نَّهْدِي بِهِۦ مَن نَّشَآءُ مِنْ عِبَادِنَا
وَإِنَّكَ لَتَهْدِي إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿49﴾ صِرَٰطِ اللَّهِ الَّذِي لَهُۥ
مَا فِي السَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ أَلَا إِلَى اللَّهِ تَصِيرُ الْأُمُورُ ﴿50﴾

43 سُورَةُ الزُّخْرُفِ مَكِّيَّةٌ
وَهِيَ تِسْعٌ وَثَمَانُونَ ءَايَةً 89

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

حمٓ وَالْكِتَٰبِ الْمُبِينِ ﴿1﴾ إِنَّا جَعَلْنَٰهُ قُرْءَٰنًا عَرَبِيًّا لَّعَلَّكُمْ
تَعْقِلُونَ ﴿2﴾ وَإِنَّهُۥ فِي أُمِّ الْكِتَٰبِ لَدَيْنَا لَعَلِيٌّ حَكِيمٌ ﴿3﴾ أَفَنَضْرِبُ
عَنكُمُ الذِّكْرَ صَفْحًا إِن كُنتُمْ قَوْمًا مُّسْرِفِينَ ﴿4﴾ وَكَمْ أَرْسَلْنَا
مِن نَّبِيٍّ فِي الْأَوَّلِينَ ﴿5﴾ وَمَا يَأْتِيهِم مِّن نَّبِيٍّ إِلَّا كَانُوا۟
بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿6﴾ فَأَهْلَكْنَا أَشَدَّ مِنْهُم بَطْشًا وَمَضَىٰ مَثَلُ
الْأَوَّلِينَ ﴿7﴾ وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضَ
لَيَقُولُنَّ خَلَقَهُنَّ الْعَزِيزُ الْعَلِيمُ ﴿8﴾ الَّذِي جَعَلَ لَكُمُ الْأَرْضَ
مَهْدًا وَجَعَلَ لَكُمْ فِيهَا سُبُلًا لَّعَلَّكُمْ تَهْتَدُونَ ﴿9﴾

49. Tamfar da muka aiko izuwa wa-ninka na daga manzanni, muka aiko izuwa gareka (Ya Muham-madu Sallallahu alaihi wa salla-ma), muka aiko da rai (Shine Alƙur'ani wanda zukata suke rayuwa da shi) daga al'amarinmu (wanda muka aiko izuwa gareka), kai baka ka-sance kasan gaban wahayi ga-reka meye Alƙur'ani ba, wala imani saidai mun sanyashi ran nan haske ne da muke shiriyar wanda muka ga dama daga bay-inmu, haƙiƙa kai kana shiryar-wa izuwa tafarki madaidaici (Shine addinin Musulunci).
50. Tafarkin Allah wanda mulkin sammai da ƙassaiya tabbata garshi, to jama'a izuwa Allah al'amura duka suke komawa.

Wannan Suratu Zukhrufu ce

A Makka aka saukar da ita Aya Tamanin da tara ce (89)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a lahira a keɓe

Ita Wannan Sura Ta Fara Da Zance Kan Alƙur'ani Da Munakasha Da Mushurukai Da Kafa Dalili Kan Samuwar Allah Da Sifofinsa Da Gurabansa Da Ni'imominsa Bisa Mutane Da Kididdigar -ƙaryace --ƙaryacensu Da Akididinsu Batattu Da Raddi Akansu Da Abindazai Kwabesu Da Kafa Dalili Da Ba'alin Annabawa Kamar Annabi Musa Da Haluluwa Ranar Alƙiyama Dangane Da Muminai Da Kafirai da Hikimomin Alƙur'ani Da Wadansunsu.

(ALƘUR'ANI MAI HIKIMA DA KURAISHU)

1. Allahu a'alamu bimuradihi bi zalika, Ubangiji yayi rantsuwa da alƙur'ani mai bayyana (han-yar gaskiya da abinda ake bukata gareshi na shari'a).
2. Haƙiƙa mu mun sanya wannan alƙur'ani Balarabe sabodaku ,mutanen Makka ku fahimci ma'anoninsa (wato Kuraishu).
3. Haƙiƙa shi abin tabbatarwa ne a cikin uwar littattafai (Lauhil Mahfuzu) nan garemu, lallai madaukaki ne kan littattafai hik-ima ne wacce ta isa matuka.
4. To shin ma r'ike alƙur'ani ga bu-ran ku rikewa (Baza ayi muku umarni ko hani baku zama ka-mar dabbobi) don kun kasance mutane mushurikai? (A'a).
5. Da yawa muka aiko Annabi cikin mutanen farko.
6. Ba wani Annabi dayazo musu face sun kasance masu izigili dashi, (kamar da mutanenka suke izgili da kai, wannan rarraShine ga Sallallahu alaihi wa sallama).
7. Muka halakar da mafi tsananin karfi (wato danka) daga muta-nen ka misalin mutanen farko (wato sifar su a cikin halakar-wa) ya shude, ƙarshen mutanen ka kamar haka zai kasance).

(DAGA NI'IMOMIN ALLAH A GAREMU)

8. Wallahi in ka tambaye su waya halicci sammai da ƙassai lallai zasu ce Ubangiji mabuwayi Shine ya habicce su mabuwayi mai cikakken sani (kuma Ubangiji ya R-ara da cewa).
9. Shine wahda sanya ƙasa shim-fida a gare ku, (kamar gadon ja-riri) yasanya muku tafarkuna a cikinta don ku sami shiriya (cikin tafiye-tafiyenku).

وَالذِے نَزَّلَ مِنَ اَ۬لسَّمَآءِ مَآءَۢ بِقَدَرٖ فَأَنشَرْنَا بِهِۦ بَلْدَةٗ مَّيْتاٗۖ
كَذَٰلِكَ تُخْرَجُونَۖ (10) * وَالذِے خَلَقَ اَ۬لْأَزْوَاجَ كُلَّهَا وَجَعَلَ ثمن
لَكُم مِّنَ اَ۬لْفُلْكِ وَالْأَنْعَٰمِ مَا تَرْكَبُونَ (11) لِتَسْتَوُۥاْ عَلَيٰ ظُهُورِهِۦ
ثُمَّ تَذْكُرُواْ نِعْمَةَ رَبِّكُمْ إِذَا اَ۪سْتَوَيْتُمْ عَلَيْهِ وَتَقُولُواْ سُبْحَٰنَ
اَ۬لذِے سَخَّرَ لَنَا هَٰذَا وَمَا كُنَّا لَهُۥ مُقْرِنِينَ (12) وَإِنَّا إِلَيٰ
رَبِّنَا لَمُنقَلِبُونَۖ (13) وَجَعَلُواْ لَهُۥ مِنْ عِبَادِهِۦ جُزْءاًۖ
إِنَّ اَ۬لْإِنسَٰنَ لَكَفُورٞ مُّبِينٌۖ (14) أَمِ اِ۪تَّخَذَ مِمَّا يَخْلُقُ بَنَٰتٖ
وَأَصْفَيٰكُم بِالْبَنِينَۖ (15) وَإِذَا بُشِّرَ أَحَدُهُم بِمَا ضَرَبَ لِلرَّحْمَٰنِ مَثَلاٗ
ظَلَّ وَجْهُهُۥ مُسْوَدّاٗ وَهْوَ كَظِيمٌۖ (16) أَوَمَنْ يُنَشَّؤُاْ فِے اِ۬لْحِلْيَةِ
وَهْوَ فِے اِ۬لْخِصَامِ غَيْرُ مُبِينٖۖ (17) وَجَعَلُواْ اُ۬لْمَلَٰٓئِكَةَ اَ۬لذِينَ
هُمْ عِندَ اَ۬لرَّحْمَٰنِ إِنَٰثاًۖ أَ۬وُشْهِدُواْ خَلْقَهُمْۖ سَتُكْتَبُ شَهَٰدَتُهُمْ
وَيُسْـَٔلُونَۖ (18) وَقَالُواْ لَوْ شَآءَ اَ۬لرَّحْمَٰنُ مَا عَبَدْنَٰهُمۖ
مَّا لَهُم بِذَٰلِكَ مِنْ عِلْمٍۖ اِنْ هُمُۥ إِلَّا يَخْرُصُونَۖ (19) أَمَ اٰتَيْنَٰهُمْ
كِتَٰباٗ مِّن قَبْلِهِۦ فَهُم بِهِۦ مُسْتَمْسِكُونَۖ (20) بَلْ قَالُوٓاْ إِنَّا
وَجَدْنَآ ءَابَآءَنَا عَلَيٰٓ أُمَّةٖ وَإِنَّا عَلَيٰٓ ءَاثٰ۪رِهِم مُّهْتَدُونَۖ (21)

10. Shine wanda ya saukar da ruwa daga sama gwargwadon buka-tarku, (wato bamu saukar dashi kamar ruwan dufanu ba), muka raya birni ReKashashshe dashi (ruwan) kamar haka ake fitar da ku (daga cikin Raburbura rayayyu).
11. Shine wanda ya halicci nau'o'i dukkanta (kamar zaRi da tsami da fari da baRi da namiji da mace da saurar irinsu), yasanya muku abubuwan da kuke hawa Shine jiraga da dabbobi (kamar raRuma da dawakai).
12. Domin kuyi daidai a kan bayan-ta sannan ku anbaci ni'imar Ubangijinku inkun daidai a kanta, ku ce, "Tsarki ya tabba-tarwa wanda ya hore wannan garemu, bamu kasance masu samun iko a gareshi ba".
13. " Hakika mu masu komawa ne izuwa Ubangijinmu".

(NAU'O'I NA DAGA KARAIRAYINSU DA RADDI A KANSU)

14. Sun sanyajizi'i gareshi daga bayinsa, (sun sanya masa wani yanki daga bayinsa, lokacin da sukace Mala'iku 'ya'yan Allah ne domin da jizi'in ubane, Mala'iku ko bayin Allah ne), shi dai mutum (wanda yake faɗan wannan magana) mai ka-. firci ne mabayyanin kafirci.
15. Shin kwa dinga cewa, "yariki 'ya'yaye mata daga abinda ya halitta?Ya tsarkake kuda ma-zaje?"
16. Idan an yiwa dayansu albishir da abinda ya sabanya misali dashi ga Ubangiji sai fuskarsa ta zama bakikkirin alhali shi yana mai hadlye fushi, (yaya yake danga-na 'ya'ya mata izuwa Allah, Allah ya girma ga buran wannan).
17. Yanzu sa sanyaga Allah wanda ake tashinsa a cikin ado alhali shi a cikin husuma bazai iya bayyana hujja ba (saboda rau-ninsa na matantaka).
18. Sun sanya Mala'iku mata, waɗandasu bayin Ubangiji ne, sun halarci halittar su ne? Da sannu zamuyi umarnin rubuta shaidarsu (da cewa su mutane ne), kuma za a tambaye su a ra-nar lahira (kuma ayi musu ukuba a kanta).
19. Sai sukace, "Da Ubangiji Ar-rahmanu dayaga dama da bazamu bautawa waɗannan Mala'iku ba (to bautan nan ta mu*ga Mala'ikuda nufin Allah ne, to shiya yarda ne da ita. Sai Ubangiji ta'ala yace) basu da sani da wancanenka, basu da wani ilimi da wannan magana na bauta mata, su basu sani ba face Rarya ne kawai, (sai ayi musu azaba a kanta).
20. Shin mun basu littafi ne gaban alkur'ani da bautar wanin Allah, suke rike dashi? (A'a).
21. Bari! Sunce "Mun samu iyay-enmu a kan addini, hakika mu masu bi ne a kan guraban su, sun kasance suna bautawa wa-nin Allah.

وَكَذَٰلِكَ مَآ أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ فِى قَرْيَةٍ مِّن نَّذِيرٍ إِلَّا قَالَ
مُتْرَفُوهَآ إِنَّا وَجَدْنَآ ءَابَآءَنَا عَلَىٰٓ أُمَّةٍ وَإِنَّا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم مُّقْتَدُونَ ﴿22﴾
* قَٰلَ أَوَلَوْ جِئْتُكُم بِأَهْدَىٰ مِمَّا وَجَدتُّمْ عَلَيْهِ ءَابَآءَكُمْ حزب
قَالُوٓاْ إِنَّا بِمَآ أُرْسِلْتُم بِهِۦ كَٰفِرُونَ ﴿23﴾ فَانتَقَمْنَا مِنْهُمْ فَانظُرْ
كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ الْمُكَذِّبِينَ ﴿24﴾ وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِيمُ لِأَبِيهِ
وَقَوْمِهِۦٓ إِنَّنِى بَرَآءٌ مِّمَّا تَعْبُدُونَ ﴿25﴾ إِلَّا الَّذِى فَطَرَنِى فَإِنَّهُۥ
سَيَهْدِينِ ﴿26﴾ وَجَعَلَهَا كَلِمَةًۢ بَاقِيَةً فِى عَقِبِهِۦ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿27﴾
بَلْ مَتَّعْتُ هَٰٓؤُلَآءِ وَءَابَآءَهُمْ حَتَّىٰ جَآءَهُمُ الْحَقُّ وَرَسُولٌ
مُّبِينٌ ﴿28﴾ وَلَمَّا جَآءَهُمُ الْحَقُّ قَالُواْ هَٰذَا سِحْرٌ وَإِنَّا بِهِۦ كَٰفِرُونَ ﴿29﴾
وَقَالُواْ لَوْلَا نُزِّلَ هَٰذَا الْقُرْءَانُ عَلَىٰ رَجُلٍ مِّنَ الْقَرْيَتَيْنِ عَظِيمٍ ﴿30﴾
أَهُمْ يَقْسِمُونَ رَحْمَتَ رَبِّكَ نَحْنُ قَسَمْنَا بَيْنَهُم مَّعِيشَتَهُمْ
فِى الْحَيَوٰةِ الدُّنْيَا وَرَفَعْنَا بَعْضَهُمْ فَوْقَ بَعْضٍ دَرَجَٰتٍ لِّيَتَّخِذَ بَعْضُهُم
بَعْضًا سُخْرِيًّا وَرَحْمَتُ رَبِّكَ خَيْرٌ مِّمَّا يَجْمَعُونَ ﴿31﴾ وَلَوْلَآ أَن
يَكُونَ النَّاسُ أُمَّةً وَٰحِدَةً لَّجَعَلْنَا لِمَن يَكْفُرُ بِالرَّحْمَٰنِ
لِبُيُوتِهِمْ سُقُفًا مِّن فِضَّةٍ وَمَعَارِجَ عَلَيْهَا يَظْهَرُونَ ﴿32﴾

22. To haka nan, a gabanka bamu aiko wani mai gargaɗi a cikin wata alkaryaba face sai mani'imtanta sun faɗi magana irin maganar mutanenka, " Haƙiƙa mu mun sami iyayen-mu a kan addini, haƙiƙa mu masu bi ne bisa gurabansu".
23. Cene (dasu) "kwa dinga bin wancanenka koda nazo mukuda mafi shiriya daga abinda kuka sami iyayenku a kansa", sukace, "hakiK.a mu mun karfice da abinda aka aiko ka dashi (kai da magabatanka").
24. Sai mukayi damka a garesu, ka dubaka gani kaka ƙarshen masu ƙaryatawa ta kasance?.

(MUSUNSU ANNABCI DA RADDI A KANSU DA BAYANIN WULARANCIN DUNIYA)

25. Ambaci zamanin da Annabi Ib-rahim ya ambata ga mutanensa, haƙiƙa ni makubuci ne daga abinda kuke bautawa.
26. Sai wanda ya halicce ni, haƙiƙa shi da sannu zai shirye ni.
27. Yasanya ita (wannan kalma ta tauhida wacce aka fahimta daga fadinsa, "ni matafiyi ne izuwa Ubangiji da sannu zai shirye ni", yasanya ta) kalma mai '--wanzuwa a cikin zuriya tasa, (wandazai kadaita Allah bazai kau ba a cikinsu har izuwa ta-shin alƙiyama), saboda su muta-nen Makka su komo (ga buran abinda suke kansa izuwa addi-nin Annabi Ibarahim uban su).
28. Bari! Na jiyar da waɗannan mu-shurikai dadi dasu da iyayensu (ba musu garaje da ukuba ba) har alkuran yazo musu da man-zo mai bayyana musu hukunce-hukuncen shari'a (Shine Annabi Sallallahu alaihi wa sallama).
29. Yayin da gaskiya yazo musu (wato alƙur'ani) sai sukace, wannan tsafi ne, mu masu kafiri cewadaShine".
30. Sukace, "Saboda me ba a sauk-ar da wannan alƙur'ani a bisa mutum mai girma a bisa alkaryatun nan guda biyu ba (Daga kowace ɗaya daga garesu, Walidu dan Magira a Makka, ko Uwartu dan Masudu Assakafi a Da'ifa? [1].
31. Shin sune suke raba rahamar Ubangijinka (wato Annabci) mune muka raba arzikinsu a tsaka-hinsu a cikin rayuwar duniya, (muka sanya ba'alinsu ganiya), muka daukaka ba'alinsu da wadata burbushin ba'ali da dar-ajoji, don ba'alinsu (mawadaci) ya riki ba'ali (fakiri ya rike shi) abin horewa (cikin aiki yayi masa aiki da lada), Rahamar Ubangijinka (aljanna) ita tafi daga abinda suke tarawa a duniya.
32. Ba don kada mutane su zama al'umma ɗaya (a kan kafirci ba) da mun sanyaga wanda yake kafircewa ga LJbangijinsa, rufi ga dakunansu na azurfa da tsan-unuwa na azurfa da zasu hau •izuwa kan bene a kanta.

1) Shi Uwartu dan AssaRafi ya Musuiunta, Mu-suluncinsa yayi kyau, Annabi Sallallahu alaihi wa sallama yana kwatantashi da An-nabi Isa, amma Walidu dan Magira bai musu-lunta ba, Allah ya kiyashemu, Amin. Sanajiy-

وَلِبُيُوتِهِمْ أَبْوَٰبًا وَسُرُرًا عَلَيْهَا يَتَّكِـُٔونَ ﴿33﴾ وَزُخْرُفًا
وَإِن كُلُّ ذَٰلِكَ لَمَا مَتَٰعُ الْحَيَوٰةِ الدُّنْيَا وَالْأَخِرَةُ عِندَ
رَبِّكَ لِلْمُتَّقِينَ ﴿34﴾ وَمَن يَعْشُ عَن ذِكْرِ الرَّحْمَٰنِ نُقَيِّضْ لَهُۥ شَيْطَٰنًا
فَهُوَ لَهُۥ قَرِينٌ ﴿35﴾ وَإِنَّهُمْ لَيَصُدُّونَهُمْ عَنِ السَّبِيلِ وَيَحْسِبُونَ
أَنَّهُم مُّهْتَدُونَ ﴿36﴾ حَتَّىٰ إِذَا جَآءَانَا قَالَ يَٰلَيْتَ بَيْنِي وَبَيْنَكَ
بُعْدَ الْمَشْرِقَيْنِ فَبِئْسَ الْقَرِينُ ﴿37﴾ وَلَن يَنفَعَكُمُ الْيَوْمَ
إِذ ظَّلَمْتُمْ أَنَّكُمْ فِي الْعَذَابِ مُشْتَرِكُونَ ﴿38﴾ أَفَأَنتَ تُسْمِعُ
الصُّمَّ أَوْ تَهْدِي الْعُمْيَ وَمَن كَانَ فِي ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿39﴾
فَإِمَّا نَذْهَبَنَّ بِكَ فَإِنَّا مِنْهُم مُّنتَقِمُونَ ﴿40﴾ أَوْ نُرِيَنَّكَ
الَّذِي وَعَدْنَٰهُمْ فَإِنَّا عَلَيْهِم مُّقْتَدِرُونَ ﴿41﴾ * فَاسْتَمْسِكْ
بِالَّذِي أُوحِيَ إِلَيْكَ إِنَّكَ عَلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿42﴾ وَإِنَّهُۥ لَذِكْرٌ
لَّكَ وَلِقَوْمِكَ وَسَوْفَ تُسْـَٔلُونَ ﴿43﴾ وَسْـَٔلْ مَنْ أَرْسَلْنَا مِن
قَبْلِكَ مِن رُّسُلِنَا أَجَعَلْنَا مِن دُونِ الرَّحْمَٰنِ ءَالِهَةً يُعْبَدُونَ ﴿44﴾
وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا مُوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَا إِلَىٰ فِرْعَوْنَ وَمَلَإِيْهِۦ فَقَالَ إِنِّي
رَسُولُ رَبِّ الْعَٰلَمِينَ ﴿45﴾ فَلَمَّا جَآءَهُم بِـَٔايَٰتِنَا إِذَا هُم مِّنْهَا يَضْحَكُونَ ﴿46﴾

ثمن

33. Kuma (da mun sanya) kyamare (na azurfa) ga gidaddajinsu, kuma (mu sanya musu gadaje (na azurfa), su dinga dogaro a kanta.
34. Da zinariya, (Ma'ana wannan rufi da kyamare da tsanunuwa duk su zama na zinariya, wato ba don muna tsoratar kafirtar mumini ba, saboda baiwa kafiri abinda muka ambato da sai mu badashi gareshi wato ga kafirin saboda rashin girman duniya a gurinmu, da rashin rabonsa a lahira), dukkan wancanenka bai zamo ba, sai dan amfanin rayu-war duniya. Lahira (wato aljan-narka) ta tabbata ga masu jin tsoron Allah.
35. Wanda ya bijire ga buran anba-ton Ubangijinsa (wato alƙur'ani da waninsa) zamu hukunta masa shaiɗan, shi shaiɗan ya zama aboki gareshi (bazai rabu dashi) ba.
36. Haƙiƙa su (shaiɗanu) suna kaw-ar da masu bijirewan nan ga bu-ran hanya, kuma suna zaton su shiryayyu ne su.
37. Har yayin da mai bijirewan nan yazo mana (a ranar alƙiyama) sai yace dashi, "ina ma tsaka-nina da tsakanln ka akwai nisan (tsakanin) mahudar rana da maɓadarta, kai tur! aboki kai ga-reni".
38. (Ubangiji ta'ala yace), "Ku masu bijicewa ga buran anbato-na, nadamar ku bazata anfane ku ba a yau, don zalincin ku ya bayyana (da mushurikanci a du-niya), haƙiƙa kuda abokanku kuna tattare cikin azaba".

(KARFAFA KUDURIN ANIYA)

39. Shin to kai ka jiyar da kurame ko ka shiryi makafi bayan sun kasance a cikin bata mabayyani? (Waɗannan bazasu bada gaskiya ba).
40. To in muka tafiyar dakai (muka karɓi ranka) tun gaban bamu yi musu azaba ba, to haƙiƙa mu masuyin azabane garesu a ra-nar lahira.
41. Ko muka nuna maka abinda mukayi musu alkawari dashi (na azaba a ranar lahira), to haƙiƙa mu masu ikone bisayi musu azaba.
42. Kai dai ka kankame abinda ka aiko dashi izuwa gareka (na alƙur'ani), haƙiƙa kai kana kan tafarki madaidaici.
43. Haƙiƙa shi daukaka ne gareka da mutanenka (donya sauka da harshensu), da sannu za a tam-baye ku a kan tsayawa da hakkinsa.
44. Ka tambayi waɗanda muka aiko gabanka na manzanni, shin mun sanya iyayen giji da ake bauta musu ba Allah ba? (Ance an tat-tara masa manzannine daren Isra'i ko kuma Ance ne ya tam-bayi wadansu al'ummatai ne daga ma'abota littafi, to ta kow-ane hali dai bai tambaya ba, do-min abinda ake nufi da umarnin tambayo saboda tabbatarwa Ku-raishu, cewa wani jakada ko lit-tafi bai zo ba wanin Allah basu ma kuma sun gamsu da wan-nan).

(IZNA DA ƘISSAR ANNABI MUSA ALAIHAISSALAMU DA FIR'AUNU)

45. Haƙiƙa mun aiki Annabi Musa da ayoyinmu izuwa Fir'auna da mutanensa (Kibdawa) sai yace, " Haƙiƙa ni manzon Ubangijin talikai ne".
46. Yayin dayazo musu da ayoyin-mu (da aikenmu) sai gasu suna dariya daga gareta.

وَمَا نُرِيهِم مِّنْ ءَايَةٍ إِلَّا هِيَ أَكْبَرُ مِنْ أُخْتِهَا وَأَخَذْنَاهُم
بِالْعَذَابِ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿47﴾ وَقَالُوا يَا أَيُّهَ السَّاحِرُ ادْعُ لَنَا
رَبَّكَ بِمَا عَهِدَ عِندَكَ إِنَّنَا لَمُهْتَدُونَ ﴿48﴾ فَلَمَّا كَشَفْنَا عَنْهُمُ
الْعَذَابَ إِذَا هُمْ يَنكُثُونَ ﴿49﴾ وَنَادَىٰ فِرْعَوْنُ فِي قَوْمِهِ
قَالَ يَا قَوْمِ أَلَيْسَ لِي مُلْكُ مِصْرَ وَهَٰذِهِ الْأَنْهَارُ تَجْرِي مِن تَحْتِي
أَفَلَا تُبْصِرُونَ ﴿50﴾ أَمْ أَنَا خَيْرٌ مِّنْ هَٰذَا الَّذِي هُوَ مَهِينٌ ﴿51﴾
وَلَا يَكَادُ يُبِينُ ﴿52﴾ فَلَوْلَا أُلْقِيَ عَلَيْهِ أَسْوِرَةٌ مِّن ذَهَبٍ
أَوْ جَاءَ مَعَهُ الْمَلَائِكَةُ مُقْتَرِنِينَ ﴿53﴾ فَاسْتَخَفَّ قَوْمَهُ
فَأَطَاعُوهُ إِنَّهُمْ كَانُوا قَوْمًا فَاسِقِينَ ﴿54﴾ فَلَمَّا ءَاسَفُونَا
انتَقَمْنَا مِنْهُمْ فَأَغْرَقْنَاهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿55﴾ فَجَعَلْنَاهُمْ سَلَفًا
وَمَثَلًا لِّلْآخِرِينَ ﴿56﴾ وَلَمَّا ضُرِبَ ابْنُ مَرْيَمَ مَثَلًا إِذَا قَوْمُكَ
مِنْهُ يَصُدُّونَ ﴿57﴾ وَقَالُوا ءَآلِهَتُنَا خَيْرٌ أَمْ هُوَ مَا ضَرَبُوهُ
لَكَ إِلَّا جَدَلًا بَلْ هُمْ قَوْمٌ خَصِمُونَ ﴿58﴾ إِنْ هُوَ إِلَّا عَبْدٌ
أَنْعَمْنَا عَلَيْهِ وَجَعَلْنَاهُ مَثَلًا لِّبَنِي إِسْرَاءِيلَ ﴿59﴾ وَلَوْ نَشَاءُ
لَجَعَلْنَا مِنكُم مَّلَائِكَةً فِي الْأَرْضِ يَخْلُفُونَ ﴿60﴾

47. Bama nuna musu wata aya badaga ayoyin azaba (kamar Du-fanu, wato ruwan ɗa ya shiga dakunansu ya sadu izuwa makogwaron mazauna kwana bakwai, face ita tafi yar uwarta girma, mun dankesu da azabasaboda su koma (ga buran kafir-ci).
48. Sai suka faɗa ga Annabi Musa yayin da suka ga azaba, "ya kai tsafau, (wato gwani a cikin tsa-fi) rokar mana Ubangijinka sa-boda abinda yayi alkawari nan gareka (na daga yaye azaba ga buran mu in mun bada gaskiya), haƙiƙa mu lallai masu shiriya ne".
49. Yayin da muka yaye azaba ga buransu (saboda addu'ar Anna-bi Musa, kumfa sai gasu suna warware alkawarinsu (suna zar-cewa kan kafircinsu).
50. Fir'auna yayi shela a cikin mu-tanensa yace, "Yaku mutanena shin mulkin Misra ba nawa bane, waɗannan ƙoramu (na Nil) suna gudana ƙarƙashina, shin ba kwa ganin (girmama ?).
51. "Ko (kuna ganin, to yayin nan) nine na fi daga wannan (wato Annabi Musa), wanda yake shi rarrauna ne wulaƙantacce".
52. Bazai kusa ya bayyana (zancen-sa basaboda guragura ta garwa-shin •daya jefa ta a bakinsa a lokacin kuruciyarsa?) to me ya sa a basaukar masa da kwandagai na zinariya ba?.
53. Ko yazo Mala'iku suna tare dashi.
54. Sai (Fir'auna) ya raina mutanen-sa sai suka daka tasa, sai sukabi shi (cikin abinda yake nufi na daga ƙaryata Annabi Musa) haƙiƙa su sun ƙasance mutane ne fasikai.
55. Zamanin da suka tsokano fu-shinmu sai muka danke su da azaba muka nutsar dasu baki ɗaya.
56. Sai muka sanya su marigaya, muka sanya su misali ga muta-nen karshe (suyiizna ga abinda ya faru garesu bazasuyiaiki irin nasu ba).

(BA'ALIN ƘARYACE-ƘARYACENSU DA RADDIKANTA)

57. Zamanin da aka sanya Annabi Isa misali, (a cikin faɗin Ubangiji kuda abinda kuke bautawa ba Allah ba gumaguman jahan-nama ne, sai mushurikai sukace, "mun yarda iyayen gijinmu su kasance tareda Annabi Isa domin shi an bauta masa ba Allah ba)". Sai ga mutanenka (mu-shurikai) suna dariya daga wan-nan misali da aka sanya musu.
58. Sukace, "iyayen gijinmune sukafi ko Annabi Isa ne yafi? Basu sanya maka misalin basai don husuma (da jayayya ta ƙarya Don sun , san cewa (MA) ana yin anfani da ita ne ga wa-nin mai hankali, Annabi Isa bazai shiga cikinta ba), barsu, mu-tane ne masu tsananin husuma.
59. Shi Annabi Isa bai kasance ba face bawa da mukayi ni'ima a gareshi (da Annabci), muka san-ya shi samamme bada uba ba), muka sanyashi misali ga Bani Isra'ila, (an sanyashi misali sa-boda balomcinsa da kafa dalili dashi bisa ikon Allah, kan abinda yake nufi).
60. Da mun ga dama da sai mu san-ya Mala'iku a bayan ƙasa (su maye maku a madadinku (mu halakar da ku).

ربع

وَإِنَّهُۥ لَعِلْمٌ لِّلسَّاعَةِ فَلَا تَمْتَرُنَّ بِهَا وَاتَّبِعُونِ هَٰذَا صِرَاطٌ
مُّسْتَقِيمٌ ﴿61﴾ وَلَا يَصُدَّنَّكُمُ الشَّيْطَٰنُ إِنَّهُۥ لَكُمْ عَدُوٌّ
مُّبِينٌ ﴿62﴾ * وَلَمَّا جَآءَ عِيسَىٰ بِالْبَيِّنَٰتِ قَالَ قَدْ جِئْتُكُم بِالْحِكْمَةِ
وَلِأُبَيِّنَ لَكُم بَعْضَ الَّذِے تَخْتَلِفُونَ فِيهِ
فَاتَّقُوا اللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿63﴾ إِنَّ اللَّهَ هُوَ رَبِّے وَرَبُّكُمْ
فَاعْبُدُوهُ هَٰذَا صِرَاطٌ مُّسْتَقِيمٌ ﴿64﴾ فَاخْتَلَفَ الْأَحْزَابُ
مِنۢ بَيْنِهِمْ فَوَيْلٌ لِّلَّذِينَ ظَلَمُوا مِنْ عَذَابِ يَوْمٍ أَلِيمٍ ﴿65﴾
هَلْ يَنظُرُونَ إِلَّا السَّاعَةَ أَن تَأْتِيَهُم بَغْتَةً وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿66﴾
الْأَخِلَّآءُ يَوْمَئِذِۢ بَعْضُهُمْ لِبَعْضٍ عَدُوٌّ إِلَّا الْمُتَّقِينَ ﴿67﴾
يَٰعِبَادِے لَا خَوْفٌ عَلَيْكُمُ الْيَوْمَ وَلَا أَنتُمْ تَحْزَنُونَ ﴿68﴾
الَّذِينَ ءَامَنُوا بِـَٔايَٰتِنَا وَكَانُوا مُسْلِمِينَ ﴿69﴾ ادْخُلُوا الْجَنَّةَ أَنتُمْ
وَأَزْوَٰجُكُمْ تُحْبَرُونَ ﴿70﴾ يُطَافُ عَلَيْهِم بِصِحَافٍ مِّن ذَهَبٍ
وَأَكْوَابٍ وَفِيهَا مَا تَشْتَهِيهِ الْأَنفُسُ وَتَلَذُّ الْأَعْيُنُ وَأَنتُمْ
فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿71﴾ وَتِلْكَ الْجَنَّةُ الَّتِے أُورِثْتُمُوهَا بِمَا كُنتُمْ
تَعْمَلُونَ ﴿72﴾ لَكُمْ فِيهَا فَٰكِهَةٌ كَثِيرَةٌ مِّنْهَا تَأْكُلُونَ ﴿73﴾

61. Hakika shi Annabi Isa ilimi ne na tashin alkiyama (za a santada saukowarsa) kada kuyi ko-konto a cikinta, ka faɗa garesu "Kubini (kan tauhudi), wannan (abinda na umarce ku dashi) tafarki ne madaidaici.
62. Kada shaiɗan ya juyar daku ,ga buran alherin Allah, saboda shi makiyi ne gareku mabayyanin kiyayya,
63. Yayin da Annabi Isa yazoda hujjoji mabayyana (wato mu'ujiza da shari'a) sai yace, " Hakika nazo mukuda sha-ri'o'i da hikima (wato Annabci da shari'un Injila) don in yi muku bayanin ba'alin abinda kuke sabawa cikinsa (na hu-kunce-hukuncen Addini da wa-ninsa, saiya bayyana musu al'amarin addini), kuji tsoron Allah kubi ni.
64. " Hakika Allah ne Ubangiji, Allah ne Ubangijinku ku bauta masa, wannan tafarki ne madai-daici".
65. Sai kungiyoyinsu suka sassabadaga tsakaninsu a cikin Annabi Isa (Shi Allah ne ko dan Allah ko na ukun uku ne, Bone ta tab-bata ga waɗanda suka kafirta (da abinda suka faɗa cikin Annabi Isa) na azabar rana mai raɗaɗi.
66. Kafiran Makka basa sauraro sai alkiyama tazo musu a rabe alha-li su basu san (lokacin zuwanta ba).

(SHASHIN HALULUWA RANAR ALKIYAMA)

67. Abokai (cikin sabon Allah a du-niya) a ranar lahira, shashinsu magauci ne ga shashi sai masu tsoron Allah kodai. (Masu soyayya a cikinsa, masu gama kai a cikin da'arsa, to su abokan juna ne ana cewa dasu).
68. "Yaku bayina ba tsoro gareku a yau, ku bazakuyi bakin ciki ba" [1]
69. " Waɗanda suka ba gaskiya da ayoyinmu (da alkur'ani) suka zama masu tsarkakewa (a cikin addini)".
70. "Ku shiga Aljanna kuda matay-enku ana faranta muku zuciya (ana girmama ku").
71. Ana kewayo a garesu da kabbuka na zinare da funjalai abinda rayuka take marmari yana cikinta idanu suke jin dadi dangane da duba, ku masu dauwama ne a cikinta.
72. Wancanenku aljanna ce wacce aka gada muku ita saboda abinda kuke aikatawa.
73. Kayan marmari na gareku a cikinta masu yawa kuna ci daga gareta (duk abinda aka ci mai- makonsa saiya maye, wato ba giɓi a aljanna).

1) A cikin Sawi yan farfajiyar aljanna saisu daga kansu saboda haka sai mai kira yace wadan-da suka bada gaskiya da ayoyinmu suka ka-sance Muusulmi sai masu addinai su sun-kuyar da wuyansu, sai Musulmi su baiyana kansu a tsaye. -Sawi-

إِنَّ ٱلْمُجْرِمِينَ فِي عَذَابِ جَهَنَّمَ خَٰلِدُونَ ﴿74﴾ لَا يُفَتَّرُ عَنْهُمْ وَهُمْ
فِيهِ مُبْلِسُونَ ﴿75﴾ وَمَا ظَلَمْنَٰهُمْ وَلَٰكِن كَانُواْ هُمُ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿76﴾
وَنَادَوْاْ يَٰمَٰلِكُ لِيَقْضِ عَلَيْنَا رَبُّكَ قَالَ إِنَّكُم مَّٰكِثُونَ ﴿77﴾ لَقَدْ جِئْنَٰكُم
بِالْحَقِّ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَكُمْ لِلْحَقِّ كَٰرِهُونَ ﴿78﴾ أَمْ أَبْرَمُواْ أَمْرًا
فَإِنَّا مُبْرِمُونَ ﴿79﴾ أَمْ يَحْسِبُونَ أَنَّا لَا نَسْمَعُ سِرَّهُمْ وَنَجْوَىٰهُم بَلَىٰ
وَرُسُلُنَا لَدَيْهِمْ يَكْتُبُونَ ﴿80﴾ قُلْ إِن كَانَ لِلرَّحْمَٰنِ وَلَدٌ فَأَنَا أَوَّلُ
ٱلْعَٰبِدِينَ ﴿81﴾ سُبْحَٰنَ رَبِّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ رَبِّ ٱلْعَرْشِ
عَمَّا يَصِفُونَ ﴿82﴾ فَذَرْهُمْ يَخُوضُواْ وَيَلْعَبُواْ حَتَّىٰ يَلْقَواْ يَوْمَهُمُ
ٱلَّذِي يُوعَدُونَ ﴿83﴾ * وَهُوَ ٱلَّذِي فِي ٱلسَّمَآءِ إِلَٰهٌ وَفِي ٱلْأَرْضِ إِلَٰهٌ
وَهُوَ ٱلْحَكِيمُ ٱلْعَلِيمُ ﴿84﴾ وَتَبَارَكَ ٱلَّذِي لَهُ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ
وَمَا بَيْنَهُمَا وَعِندَهُ عِلْمُ ٱلسَّاعَةِ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿85﴾
وَلَا يَمْلِكُ ٱلَّذِينَ يَدْعُونَ مِن دُونِهِ ٱلشَّفَٰعَةَ إِلَّا مَن
شَهِدَ بِالْحَقِّ وَهُمْ يَعْلَمُونَ ﴿86﴾ وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَهُمْ
لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ فَأَنَّىٰ يُؤْفَكُونَ ﴿87﴾ وَقِيلَهُ يَٰرَبِّ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ قَوْمٌ
لَّا يُؤْمِنُونَ ﴿88﴾ فَاصْفَحْ عَنْهُمْ وَقُلْ سَلَٰمٌ فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ ﴿89﴾

ثمن

74. Hak̃ik̃a masu laifi suna cikin wuta madauwama a cikinta.
75. Ba a sauwaKe azaba ga buran su, su a cikinta ababan kwabewa ne.
76. Ubangiji yace, "Bamu zalince su basaidai su sun kasance sune azzalumai".
77. Suka dora kira, "ya Maliku! (mataskacin wuta!) Ubangijinka yayi hukunci a kanmu, (ya kashe mu)" sai Ubangiji yace (Bayan shekara dubu [1000]) " hak̃ik̃a ku masu dauwama ne cikin azaba".
78. (Ubangiji yace), " hak̃ik̃a mun zo mukuda gaskiya (bisa harsh-en manzon Allah Sallallahu alaihi wa sallama) saidai ya-wancinku masu kin gaskiya ne".
79. Bari! Su kafiran Makka sun £ulla kaidi (cikin al'amarin Manzon Allah Sallallahu alaihi wa sallama), to hak̃ik̃ a mu masu Rullawan kaidin ne cikin halak-ar dasu.
80. Shin suna zaton Barna jin asirin sune da ganawar su izuwa wa-nin su da abinda suke bayya-nawa tsakanin wanin su? Kai muna jin wannan kuma jaka-dunmu masu kiyayewa suna ru-buta wancanenka nan garesu.

(KORUWAR DA DA SHARIKI GA ALLAH)

81. Cene, "In daya kasance ga Ubangiji (talcdiran) to nine far-kon mai bauta (ga dan, to ya tab-batacewa bada gareshi, saboɗa haka bautarsa ta koru).
82. Tsarki ya tabbatarwa Ubangijin sammai da k̃assai, Ubangijin Al'arshi alk̃ursiy ga buran abinda suke shirkantawa (na danga-na da gareshi).
83. Barsu su kutsa a cikin barnarsu suyiwasa cikin duniyar su har su gamu da ranar su wacce akc yi musu alkawari a cikinsa (Shine alk̃iyama).
84. Shine abin bautawa a sama Shine abin bautawa a k̃asa Shine gwani (a cikin shirin halitta tasa) masani (da masalaharsu).
85. Sarkin nan da mulkin sammai da k̃assaida abin yake tsakaninsu yake gareshi alherinsa ya dadu ya yawaita, sanin yaushe alk̃iyama zata tashi yana gare-shi, izuwa gareshi ake komo da ku.
86. Waɗanda kafirai suke bautawa ba Allah ba, basu mallaki ceto ga kowa ba, sai wanda yayi shaida da gaskiya (yace "LA ILAHA ILLALLAHU) alhali su sun sani (da zuciyarsu abinda harshensu ya shaida dashi sune Annabi Isa da Uzairu da Mala'iku, hak̃ik̃a su suna ceto ga muminai).
87. Wallahi in ka tambaye su waya halicce su? **Zasu** ce da kai, "Allah ne", to donme aka juyar dasu (ga buran bautar Allah?).
88. Ya faɗi magana tasa cewa "ya Ubangijina waɗannan mutane mutane ne da bazasu bada gaskiya ba".
89. (Ubangiji ta'ala yace, "To rabi dasu); cene "Gaisuwa daga ga reku, (wannan tun gaban ba ;umarce su dayak̃in su bane) d;sannu zaku sani, (ma'ana da sannu zaka k̃anɗana kudarku)".

44 سُورَةُ الدُّخَانِ مَكِّيَّةٌ
وَهِيَ سِتٌّ وَخَمْسُونَ ءَايَةً 56

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

حمٓ وَالْكِتَٰبِ الْمُبِينِ ﴿1﴾ إِنَّا أَنزَلْنَٰهُ فِي لَيْلَةٍ مُّبَٰرَكَةٍ
إِنَّا كُنَّا مُنذِرِينَ ﴿2﴾ فِيهَا يُفْرَقُ كُلُّ أَمْرٍ حَكِيمٍ ﴿3﴾ أَمْرًا مِّنْ عِندِنَا
إِنَّا كُنَّا مُرْسِلِينَ ﴿4﴾ رَحْمَةً مِّن رَّبِّكَ إِنَّهُ هُوَ السَّمِيعُ الْعَلِيمُ ﴿5﴾
رَبُّ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا إِن كُنتُم مُّوقِنِينَ ﴿6﴾
لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ يُحْيِي وَيُمِيتُ رَبُّكُمْ وَرَبُّ ءَابَآئِكُمُ الْأَوَّلِينَ ﴿7﴾
بَلْ هُمْ فِي شَكٍّ يَلْعَبُونَ ﴿8﴾ فَارْتَقِبْ يَوْمَ تَأْتِي السَّمَآءُ بِدُخَانٍ مُّبِينٍ ﴿9﴾
يَغْشَى النَّاسَ هَٰذَا عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿10﴾ رَّبَّنَا اكْشِفْ عَنَّا الْعَذَابَ إِنَّا
مُؤْمِنُونَ ﴿11﴾ أَنَّىٰ لَهُمُ الذِّكْرَىٰ وَقَدْ جَآءَهُمْ رَسُولٌ مُّبِينٌ ﴿12﴾
ثُمَّ تَوَلَّوْا عَنْهُ وَقَالُوا مُعَلَّمٌ مَّجْنُونٌ ﴿13﴾ إِنَّا كَاشِفُوا الْعَذَابِ
قَلِيلًا إِنَّكُمْ عَآئِدُونَ ﴿14﴾ يَوْمَ نَبْطِشُ الْبَطْشَةَ الْكُبْرَىٰ
إِنَّا مُنتَقِمُونَ ﴿15﴾ وَلَقَدْ فَتَنَّا قَبْلَهُمْ قَوْمَ فِرْعَوْنَ وَجَآءَهُمْ رَسُولٌ
كَرِيمٌ ﴿16﴾ أَنْ أَدُّوا إِلَيَّ عِبَادَ اللَّهِ إِنِّي لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿17﴾

Wannan Suratu Ddukhanu ce

A Makka aka saukar da ita Aya Hamsin Dashida ce (56)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinRan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinkan Muminai a lahira a keɓe

Ita Wannan Sura Ta Tabbatar A kan Girman AlƘur'ani Da Ba Wa Mushurikai Tsoro Da Saba Misalai Da Fir'auna Da Mutanensa Da Kareshensu Da Tabbatar Da Tashin alƙiyama Da Munakasha Dasu A Cikinta, Da Bayanin Haluluwansa Wanda ya Kebantada Kafirai Da Muminai Sannan An Cikata Kamar Yadda Aka Faratada Zance Kan AlƘur'ani.

(WANCANENKA SHINE ALƘUR'ANI)

1. Allahu a'alamu bi muradihi bi zalika, Allah yayi rantsuwa da alƘur'ani mai bayyana (haram da halal).
2. Haƙiƙa mun saukar dashi cikin dare mai albarka (daren Lailatul Kadri ko daren rabin Sha'aban, ya sauka a cikinta daga Ummil Kitabi, daga sama ta bakwai izuwa sama ta duniya), haK-ika mu mun kasance masu tsoratar-wa (dashi wannan alƙur'ani).
3. A cikin daren Lailatul Kadri ne ko daren rabin Sha'abana ake fayyacewar dukkan lamari abin ingantawa, (na daga arzuka da ajalai da waninsu wacce zata afku a wannan shekara izuwa wannan dare).
4. Don fayyacewa daga garemu. Haƙiƙa mun kasance masu aiko (manzanni Annabi Sallallahu alaihi wa sallama da waɗanda suke gabansa).
5. Don jinƙai (ga waɗanda aka aiko izuwa garesu wanda yafito) daga Ubangijinka, haJcilea Ubangijinka Shine mai ji (ga inagan-ganu da ayyuka), Shine mai sani (ga maganganunsu da ayy-ukansu).
6. Ubangiji sammai da ƙassaida abinda yake tsakaninsu inkun kasance (ku mutanen Makka) masu sakankancewa ne (a kan Shine Ubangijin sammai da ƙassai to ku sakankance cewa Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wa sallama manzonsa ne).
7. Ba abin bautawa da gaskiya sai shi, mai rayawa mai matarwa, Ubangijinku Ubangijin iyayen-ku na farko.
8. Bari! Sudai suna cikin kokonta (game da tashin alƙiyama) suna wasanni (don izgili da kai, Ya Annabi Sallallahu alaihi wa sal-lam).
9. (Sai yace, "Ubangiji ka taimake ni kansu da bakwai kamar bak-wai din Yusifa" wato shekarun fari) sai Ubangiji yace, "Ka sauriri rana wacce sama zata zoda hayaƙi mabayyani". (Sai ƙasa tashiga fari yunwa tayi tsanani dasu, har dai suka ga kamar hayaki tsakanin sama da ƙasa saboda tsananin yunwa).
10. Ya lullube mutane sai sukace "Wannan azaba ce mai raɗaɗi '.
11. "Ubangiji ka yaye mana azaba ga buranmu haƙiƙa mu masu gasgata Annabin ka ne".
12. Sai Ubangiji yace, "Yayagar-gadi garesu? (Imani bazai an-fane su ba bayan saukar azaba), haƙiƙa manzo mabayyanin aiki yazo musu".
13. Sannan suka bada bayaga bu-ransa, sai sukace, "ai almajiri ne (wanda wani mutum da ake ce dashi Bishru yake koya masa ilimi), kuma ba mai han-kali ba".
14. Haƙiƙa mu zamu yaye azaba ga buranku dan lokaci kankani (to sai aka yaye azabar ga buransu din). Haƙiƙa ku masu komawa ne (izuwa kafircinku, to sai suka koma izuwa gareshi din kuwa).
15. Ka ambaci ranar da muke yin danka, danka (Itace ranar Badar), haƙiƙa mu masuyin azabane garesu.

(SABODA ME BASA IZNA DA FIR'AUNA DA MUTANENSA)

16. Lallai mun jarrabi mutanen Fir'auna gabansa tare da Fir'auna din manzo mai girma ga Allah Shine Annabi Musa, yazo musu.
17. (Yazo musu da) ku bani abinda nake kiranku izuwa gareshi na imani (ai ku bayyana mini imaninku kuyi da'a gare ni) Yaku bayin Allah, haƙiƙa ni man-zo ne gareku amintacce (a bisa abinda aka aiko ni dashi).

وَأَن لَّا تَعْلُوا عَلَى اللَّهِ إِنِّي آتِيكُم بِسُلْطَانٍ مُّبِينٍ ﴿18﴾
وَإِنِّي عُذْتُ بِرَبِّي وَرَبِّكُمْ أَن تَرْجُمُونِ ﴿19﴾ وَإِن لَّمْ تُؤْمِنُوا لِي
فَاعْتَزِلُونِ ﴿20﴾ فَدَعَا رَبَّهُ أَنَّ هَٰؤُلَاءِ قَوْمٌ مُّجْرِمُونَ ﴿21﴾ فَأَسْرِ
بِعِبَادِي لَيْلًا إِنَّكُم مُّتَّبَعُونَ ﴿22﴾ وَاتْرُكِ الْبَحْرَ رَهْوًا
إِنَّهُمْ جُندٌ مُّغْرَقُونَ ﴿23﴾ * كَمْ تَرَكُوا مِن جَنَّاتٍ وَعُيُونٍ ﴿24﴾
وَزُرُوعٍ وَمَقَامٍ كَرِيمٍ ﴿25﴾ وَنَعْمَةٍ كَانُوا فِيهَا فَاكِهِينَ ﴿26﴾ كَذَٰلِكَ
وَأَوْرَثْنَاهَا قَوْمًا آخَرِينَ ﴿27﴾ فَمَا بَكَتْ عَلَيْهِمُ السَّمَاءُ وَالْأَرْضُ
وَمَا كَانُوا مُنظَرِينَ ﴿28﴾ وَلَقَدْ نَجَّيْنَا بَنِي إِسْرَائِيلَ مِنَ الْعَذَابِ الْمُهِينِ ﴿29﴾
مِن فِرْعَوْنَ إِنَّهُ كَانَ عَالِيًا مِّنَ الْمُسْرِفِينَ ﴿30﴾ وَلَقَدِ اخْتَرْنَاهُمْ
عَلَىٰ عِلْمٍ عَلَى الْعَالَمِينَ ﴿31﴾ وَآتَيْنَاهُم مِّنَ الْآيَاتِ مَا فِيهِ بَلَاءٌ
مُّبِينٌ ﴿32﴾ إِنَّ هَٰؤُلَاءِ لَيَقُولُونَ إِنْ هِيَ إِلَّا مَوْتَتُنَا الْأُولَىٰ وَمَا نَحْنُ
بِمُنشَرِينَ ﴿33﴾ فَأْتُوا بِآبَائِنَا إِن كُنتُمْ صَادِقِينَ ﴿34﴾ أَهُمْ خَيْرٌ
أَمْ قَوْمُ تُبَّعٍ وَالَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ أَهْلَكْنَاهُمْ إِنَّهُمْ كَانُوا مُجْرِمِينَ ﴿35﴾
وَمَا خَلَقْنَا السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا لَاعِبِينَ ﴿36﴾
مَا خَلَقْنَاهُمَا إِلَّا بِالْحَقِّ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿37﴾

ربع

18. Kada kuyi jabberanci bisa Allah (da barin da'arsa), haƙiƙa ni zan zo mukuda dalili ne mabayyani (a bisa aikena, sai suka bashi tsoro da rajamu sai yace).
19. "Ni ina neman tsari da Ubangiji-na a kan ku jefe ni da duwar-watsu".
20. "Inbakuyi imani da faɗata ba, (ma'ana inbaku gasgata ba) to ku bar cutata", (basu bar cutar tasa ba).
21. Saiya roki Ubangijinsa saboda haƙiƙa waɗannan mutane ne mushurikai, (sai Ubangiji yace).
22. "To ka tafi da bayina (Bani Isra'ila) da daddare, haƙiƙa su ababan bi ne (wato Fir'auna da mutanensa zasu bi ku).
23. Ka bar kogin (in ka yanke shi kai - da abokanka; ka bar shi) a zaune (yadda yake a bude har Kibdawa su shiga shi) don haƙiƙa su runduna ne aba-ban nutsarwa, (saiya nutsu da wancanenka sai aka nutsar dasu).
24. Da yawa suka bari na daga go-nakai da marmaru (wato idanun ruwa masu gudana).
25. Da hatsaitsaida mazauni kyak-kyawa.
26. Da 'yar more, (wato cikakkiyar morewa) da suka kasance masu ni'imtuwa a cikinta.
27. Al'amarin haka yake, muka ga-dar da ita ga mutane wadansu dabam (ba Kibdawa ba, wato Bani Isra'ila).
28. To sama ba tayi kuka a kansu bada ƙasa, (sabanin muminai, gurin sallarsu zaiyi kuka a garesu na ƙasa da mahayin aikinsu na daga sama), basu kasance ababan saurarawa (donsu tuba) ba.
29. Haƙiƙa mun tserar da Bani Isra'ila daga azaba mai wulaKantarwa (kashe 'ya'yaye da bautar da mataye).
30. Daga Fir'auna, haƙiƙa shi (Fir'auna) ya kasance Jabberi daga cikin mabarnata.
31. Haƙiƙa mun zabi Bani Isra'ila bisa cikakken sani da muke dashi da halinsu, mun fifita su a kan talikan zamaninsu, (wato mahankalta).
32. Mun basu na daga ayoyi abinda ni'ima mabayyaniya take cikinsa, (Shine kecewar kogi da darbada soyayyen tsuntsu da waninsu).

(MUSUN, TASHIN ALƘIYAMA DA RADDI A KANSU)

33. Haƙiƙa lallai waɗannan (kafiran Makka) lallai suna cewa ba wata mutuwa (wacce rayuwa take bayanta) sai mutuwar mu ta farko (alhali su suna ɗigon maniyyi), mu bamu kasance ababan tashi (bayan mutuwa ta biyu) ba.
34. Ku zoda iyayen mu rayayyu inkun kasance masu gaskiya (cewa mu za a tashe mu ranar alƙiyama).
35. Sai Ubangiji yace, "Sune sukafi ko mutanen Tubba'u (wato Shine Tubba'u! Himyari) [1] da waɗanda suke gabansu na daga al'umma, mun halakar dasu (saboda kafircinsu, wato basu kasance mafi karfi daga garesu ba an halakar dasu). Haƙiƙa su sun kasance masu laifi".
36. Bamu halicci sammai da ƙassaida abinda yake tsakaninsu muna masu wasa ba.
37. Bamu halicce su ba (su da abinda yake tsakaninsu) saida gaskiya, (domin su kafa dalili dashi bisa ikonmu), saidai yawai-cin kafiran makka basu san haka ba.

1) Tubba'ul Himyari ya gina sarmakandayanufi yaƙin Ka'abada rushe Madina aka bashi la-bari cewa ita gurin kaurar wani Annabi ne wandasunansa AHMADU saiya kame ga buransu sai yayiwa dakin Ka'aba tufa, da tu-fan burburo wato zananniya ta mutanen Yemen, ya rubuta takardaya ajiye nan ga mutanen Madina, sun kasance suna gadon wannan takarda manyaga manya har yayin da Annabi yayi hijiri izuwa garesu suka mika wannan takarda Ance wanda takardar take hannunsa a wannan lokaci Abu Ayubal Ansari, to takardar kuma zaunanniyace.,a dubasawi a duba Nasimurriyali ko sharhin Ashafa da irinsu. Ance Annabi ne, ce waliyi ne. -Sanajiy-

إِنَّ يَوْمَ الْفَصْلِ مِيقَاتُهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿٤٠﴾ يَوْمَ لَا يُغْنِي مَوْلًى عَن مَّوْلًى
شَيْئًا وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ ﴿٤١﴾ إِلَّا مَن رَّحِمَ اللَّهُ إِنَّهُ هُوَ الْعَزِيزُ الرَّحِيمُ ﴿٤٢﴾
إِنَّ شَجَرَتَ الزَّقُّومِ ﴿٤٣﴾ طَعَامُ الْأَثِيمِ ﴿٤٤﴾ كَالْمُهْلِ تَغْلِي فِي الْبُطُونِ ﴿٤٥﴾ كَغَلْيِ
الْحَمِيمِ ﴿٤٦﴾ خُذُوهُ فَاعْتِلُوهُ إِلَىٰ سَوَاءِ الْجَحِيمِ ﴿٤٧﴾ ثُمَّ صُبُّوا فَوْقَ رَأْسِهِ مِنْ
عَذَابِ الْحَمِيمِ ﴿٤٨﴾ ذُقْ إِنَّكَ أَنتَ الْعَزِيزُ الْكَرِيمُ ﴿٤٩﴾ إِنَّ هَٰذَا مَا كُنتُم بِهِ
تَمْتَرُونَ ﴿٥٠﴾ * إِنَّ الْمُتَّقِينَ فِي مَقَامٍ أَمِينٍ ﴿٥١﴾ فِي جَنَّاتٍ وَعُيُونٍ ﴿٥٢﴾ يَلْبَسُونَ
مِن سُندُسٍ وَإِسْتَبْرَقٍ مُّتَقَابِلِينَ ﴿٥٣﴾ كَذَٰلِكَ وَزَوَّجْنَاهُم بِحُورٍ عِينٍ ﴿٥٤﴾ يَدْعُونَ
فِيهَا بِكُلِّ فَاكِهَةٍ آمِنِينَ ﴿٥٥﴾ لَا يَذُوقُونَ فِيهَا الْمَوْتَ إِلَّا الْمَوْتَةَ الْأُولَىٰ وَوَقَاهُمْ
عَذَابَ الْجَحِيمِ ﴿٥٦﴾ فَضْلًا مِّن رَّبِّكَ ذَٰلِكَ هُوَ الْفَوْزُ الْعَظِيمُ ﴿٥٧﴾ فَإِنَّمَا يَسَّرْنَاهُ
بِلِسَانِكَ لَعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿٥٨﴾ فَارْتَقِبْ إِنَّهُم مُّرْتَقِبُونَ ﴿٥٩﴾

ثمن

سُورَةُ الجَاثِيَةِ مَكِّيَّةٌ 45

وَهِيَ سِتٌّ وَثَلَاثُونَ آيَةً 36

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

حمٓ ﴿١﴾ تَنزِيلُ الْكِتَابِ مِنَ اللَّهِ الْعَزِيزِ الْحَكِيمِ ﴿٢﴾ إِنَّ فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ
لَآيَاتٍ لِّلْمُؤْمِنِينَ ﴿٣﴾ وَفِي خَلْقِكُمْ وَمَا يَبُثُّ مِن دَابَّةٍ آيَاتٌ لِّقَوْمٍ يُوقِنُونَ ﴿٤﴾

38. Haƙiƙa ranar hukunci (wato ra-nar da Allah zai rabe hukunci tsakanin bayi) Itace yi musu azaba baki ɗaya (azaba madau-wamiya).
39. Ranar da uban daki bazai wada-tar da komai na (azaba) ga bu-ran bawansa ba, kuma su baza a hana musu azabar Ubangiji ba, (ranar faiyace hukuncin nan).
40. Sai wanda Allah yaji kansa (sune muminai to su shashinsu yana ceton shashi da izinin Allah), haƙiƙa shi Ubangiji ne mai rinjaye (a cikin azaba ga kafirai shi kaɗai), mai rahama (gamu-minai).
41. Haƙiƙa itaciyar zakum (Ance Itace gunar shanu. Allah zai tsiro da ita cikin tsatstsakin jahanna-ma) Itace abincin mai yawan zunubi (Abi Jahil da abokansa).
42. Kamar narkakkiyar darma mai kama da dagodagon bakin zaiti, tana tafarfasa a cikin cikkuna.
43. Kamar tafarfasar ruwa mai tsan-anin zafi.
44. (Ku Zabaniyawa) ku danke shi (shi mai yawan laifin) ku tun-kudashi izuwa tsatstsakin jahan-nama.
45. Sannan ku kwara daga burbu-shin kansa daga ruwan zafin nan.
46. Za a ce dashi, " ɗanɗani kudar ka, haƙiƙa kaine mabuwayi mai girma (a riyawarka, da fadmka babu mafi girma daga gareni a tsakanin duwarwatsunta guda biyi". Za a ce dasu).
47. " Haƙiƙa wannan abinda kuke gani, na azabar nan, Shine abinda kuke shakku a cikinsa".

(WAƊANNAN-SUNE MASU TSORON ALLAH RANAR ALƘIYAMA)

48. HaEitca masu tsoron Allah suna cikin mazauni amintacce (wan-da ba tsoro a cikinsa).
49. Cikin gonakai da idanun ruwa.
50. Suna daura tufafin sundusu (kor-en alharini) da arafiyan difaje da kakkauransa, suna masu fus-kantar juna (ba'alinsu baya du-ban keyen ba'ali, wannan ba lokacin duba izuwa Zatin Ubangiji bane, amma lokacinsa sai mu mance dukkan ni'ima.
51. Al'amarin haka yake, mun aura musu 'yan mata masu kyan idaniya masu madarar idaniyagada-gada dinta.
52. Suna kiran masu hidima a cikin aljanna dasu zo musu da dukkan abin marmari nata, suna masu amincewa (daga yanke-wartada cutarta, da dukkan tsoro).
53. Bazasu ɗanɗani mutuwa cikinta ba, bayan mutuwarsu ta farko, (ta duniya wacce ta afku garesu bayan rayuwarsu), Ubangijinsu ya kiyashe su azabar jahanna-ma.
54. Don karamci daga Ubangijinka, wancanenka Shine ainihin rabo mai girma.
55. Mudai mun sauwakewa maka alƙur'ani da lugarka (na Larabci) don Larabawa [1] su fahimce shi (daga gareka).
56. Sai ka saurari (halakarsu), haƙiƙa su masu sauraron (halakar ne, wannan tun gaban umarni dayaƙin su ne, wato mansuhi ne).

Wannan suratul Jasiyad ce

A Makka aka saukarda ita Aya Talatin dashida ce (36)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinkan talikai a duniyagaba daya, mai jin-Ean Muminai a lahira a keɓe.

Ita Wannan Sura Kamar Sauran 'yan Uwanta Ne Na Daga Surori Na Makka A Cikin Zance Kan Tauhidi Da Tabbatar Da Tashin alƙiyama Da Annabci Da Wanin Wannan Kuma Ana Rabetada Cewa Ita Sura Ce Data Fuskanci Ayoyin Allah Da Mana ki Don Nuna Ikon Allah Da Halaccin Tashin Mutane Da Gasgatacewa Alƙur'ani Zancen Allah Ne.

(ALƘUR'ANI DAGA ALLAH YAKE)

1. Allahu a'alamu bi muradihi bi zalika, saukarwar Alƙur'ani daga Allah yake mabuwayi (a cikin mulkinsa) gwani (a cikin aikinsa).
2. Haƙiƙa akwai ayoyi (masu gir-man Allah) a cikin halittar sam-mai da ƙassai ga muminai.
3. Akwai ayoyi a cikin halittarku (daga digon nudufa sannan gu-dan jini, sannan tsoka izuwa za-mowa mutum) hakana akwai a cikin abinda Allah yake daidai-tashi (a cikin ƙasa daga mai rar-rafe a kansa na mutane da wa-ninsu), ga mutane masu sakankancewa (da tashin alƙiyama).

1) Don Larabawa ko malaman Musulunci su fa-hmce shi daga gareka wata kila su sa wa'azantu su bada gaskiya. -Sanajiy -

وَاخْتِلَافِ الَّيْلِ وَالنَّهَارِ وَمَا أَنزَلَ اللَّهُ مِنَ السَّمَآءِ مِن رِّزْقٍ
فَأَحْيَا بِهِ الْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَا وَتَصْرِيفِ الرِّيَاحِ ءَايَاتٌ لِّقَوْمٍ يَعْقِلُونَ ﴿4﴾
تِلْكَ ءَايَاتُ اللَّهِ نَتْلُوهَا عَلَيْكَ بِالْحَقِّ فَبِأَيِّ حَدِيثٍ بَعْدَ اللَّهِ
وَءَايَاتِهِ يُؤْمِنُونَ ﴿5﴾ وَيْلٌ لِّكُلِّ أَفَّاكٍ أَثِيمٍ ﴿6﴾ يَسْمَعُ ءَايَاتِ اللَّهِ
تُتْلَىٰ عَلَيْهِ ثُمَّ يُصِرُّ مُسْتَكْبِرًا كَأَن لَّمْ يَسْمَعْهَا فَبَشِّرْهُ بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿7﴾
وَإِذَا عَلِمَ مِنْ ءَايَاتِنَا شَيْـًٔا اتَّخَذَهَا هُزُؤًا أُولَٰٓئِكَ لَهُمْ عَذَابٌ مُّهِينٌ ﴿8﴾
مِن وَرَآئِهِمْ جَهَنَّمُ وَلَا يُغْنِي عَنْهُم مَّا كَسَبُوا شَيْـًٔا وَلَا مَا اتَّخَذُوا مِن دُونِ
اللَّهِ أَوْلِيَآءَ وَلَهُمْ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿9﴾ ۞ هَٰذَا هُدًى وَالَّذِينَ كَفَرُوا بِـَٔايَاتِ رَبِّهِمْ
لَهُمْ عَذَابٌ مِّن رِّجْزٍ أَلِيمٌ ﴿10﴾ اللَّهُ الَّذِي سَخَّرَ لَكُمُ الْبَحْرَ لِتَجْرِيَ
الْفُلْكُ فِيهِ بِأَمْرِهِ وَلِتَبْتَغُوا مِن فَضْلِهِ وَلَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿11﴾
وَسَخَّرَ لَكُم مَّا فِي السَّمَاوَاتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ جَمِيعًا مِّنْهُ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ
لَءَايَاتٍ لِّقَوْمٍ يَتَفَكَّرُونَ ﴿12﴾ قُل لِّلَّذِينَ ءَامَنُوا يَغْفِرُوا لِلَّذِينَ لَا يَرْجُونَ
أَيَّامَ اللَّهِ لِيَجْزِيَ قَوْمًا بِمَا كَانُوا يَكْسِبُونَ ﴿13﴾ مَنْ عَمِلَ صَالِحًا فَلِنَفْسِهِ وَمَنْ أَسَآءَ
فَعَلَيْهَا ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُمْ تُرْجَعُونَ ﴿14﴾ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا بَنِي إِسْرَآءِيلَ الْكِتَابَ وَالْحُكْمَ
وَالنُّبُوءَةَ وَرَزَقْنَاهُم مِّنَ الطَّيِّبَاتِ وَفَضَّلْنَاهُمْ عَلَى الْعَالَمِينَ ﴿15﴾

رُبع

4. Akwai ayoyi ga mutane masu hankaltar dalili a cikin kai-kawon dare da rana da abinda Allah ya saukar na daga arzikin ruwa daga sama ya raya ƙasa dashi bayan ta ƙeƙashe da juyaw-an iskoki (kudu wani yayi are-wa wani yayi mai sanyi wani yayi mai zafi).
5. Wadancanenka ayoyi ababan an-bato ayoyin Allah ne, (wato huj-jojinsa ne (masu shiryarwa bisa kadaita tasa), muna bayyanata gareka, to wane zance ne kafiran Makka zasu bada gaskiya dashi? Bayan zancen Allah (Shine allair'am) da ayoyinsa (huj-jojinsa), (ai bazasu bada gaskiya ba).

(KAITO YA TABBATA GA DUKKAN MARARYACI MAI YAWAN AIKATA SAƁO

6. Azabata tabbata ga dukkan ma ,aryaci mai aikata sabo.
7. Yake jin ayoyin Allah (alfcure'ani) ana karanta ta a ga-reshi, sannan ya zarce kan kafir-cinsa, yana mai girman kai ga buran imani kamar bai taɓa jin ta ba, to yi masa albishir da azaba mai raɗaɗi.
8. Idan yasan wani abu daga ayoy-in al£ur'ani yakan riRcta abin izgili da ita, wadancanenka masu giggirbakarya, azaba mai wulaRantarwa ta tabbata garesu.
9. Jahannama tana gabansu (domin a cikin duniya suke) abinda suka tsorarta (na dukiya da aiki) bazai wadatar da komai ga bu-ran su ba, wala abinda suka riƙa ababan jibinta ba Allah ba (sune gumaka). Azaba mai gir-ma ta tabbata garesu.
10. Wannan alƙur'ani shiriya ne daga bata, waɗanda suka kafirce da ayoyin Ubangijinsu yanki na azabana garesu, na daga azaba mai raɗaɗi.

(YANA DAGA FALALAR UBANGIJI GAREMU)

11. Allah ne wanda ya hore kogi sa-boda jirage su gudana a cikinsa da izininsa, kuma don ku nema daga falalar Ubangiji (da fatau-ci) wata kila ku kwa godewa Ubangiji.
12. Kuma ya hore don ku abinda yake cikin sammai (na rana da watada taurari da ruwa da wa-ninsu) da abinda yake cikin ƙasa (na dabbada Itace da tsiri da ƙoramu da waninsa, wato ya halicci wancanenka don anfano-nin ku) baki ɗayaya hore ta ne daga gareshi, haƙiƙa lallai ak-wai ayoyi a yin tunani (a cikinta donsu bada gaskiya).
13. Ka faɗa ga wannan da suka bada gaskiya suyigafara ga waɗannan da ba tsoron basasa ta Ubangiji, (wannan gaban umar-ni dayaƙi ne), don Ubangiji ya sakawa mutane ga abinda suka kasance suna aikatawa (na daga gafartawa kafirai cutar da sukayi musu).
14. Wanda yayi aiki nagari, yayi ne don kansa, wanda ya munana to yayi ne a kansa, sannan izu-wa Ubangijinku ake komawa da ku, (a yiwa mai gyara da mai barna sakamako).

(BASU TSORO A KAN KADASU ZAMA KAMAR BANI ISRA'ILA DA UMARNINSU DA BIN SHRI'AR ALKUR'AND

15. Hatcika mun ba wa Bani Isra'ila littafin (Attaura) da hukunci (dashi a tsakanin mutane) da An-nabci (ga Annabi Musa da Ha-mna daga cikinsu), kuma mun azurta su daga dadadan haloli (kamar mannu da salwa) mun fifita su baisa masu hankalin zamaninsu.

وَءَاتَيْنَٰهُم بَيِّنَٰتٖ مِّنَ ٱلْأَمْرِ فَمَا ٱخْتَلَفُوٓاْ إِلَّا مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَهُمُ
ٱلْعِلْمُ بَغْيَۢا بَيْنَهُمْ إِنَّ رَبَّكَ يَقْضِے بَيْنَهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ فِيمَا كَانُواْ فِيهِ
يَخْتَلِفُونَ ﴿16﴾ ثُمَّ جَعَلْنَٰكَ عَلَيٰ شَرِيعَةٖ مِّنَ ٱلْأَمْرِ فَاتَّبِعْهَا وَلَا تَتَّبِعْ
أَهْوَآءَ ٱلَّذِينَ لَا يَعْلَمُونَ ﴿17﴾ إِنَّهُمْ لَن يُغْنُواْ عَنكَ مِنَ ٱللَّهِ شَيْـًٔا
وَإِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ بَعْضُهُمْ أَوْلِيَآءُ بَعْضٖ وَٱللَّهُ وَلِيُّ ٱلْمُتَّقِينَ ﴿18﴾
هَٰذَا بَصَٰٓئِرُ لِلنَّاسِ وَهُدٗى وَرَحْمَةٞ لِّقَوْمٖ يُوقِنُونَ ﴿19﴾
أَمْ حَسِبَ ٱلَّذِينَ ٱجْتَرَحُواْ ٱلسَّيِّـَٔاتِ أَن نَّجْعَلَهُمْ كَٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَوَآءٌ مَّحْيَاهُمْ وَمَمَاتُهُمْ سَآءَ
مَا يَحْكُمُونَ ﴿20﴾ وَخَلَقَ ٱللَّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ بِٱلْحَقِّ
وَلِتُجْزَيٰ كُلُّ نَفْسِۢ بِمَا كَسَبَتْ وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿21﴾
* أَفَرَأَيْتَ مَنِ ٱتَّخَذَ إِلَٰهَهُۥ هَوَيٰهُ وَأَضَلَّهُ ٱللَّهُ عَلَيٰ عِلْمٖ وَخَتَمَ عَلَيٰ سَمْعِهِۦ ثمن
وَقَلْبِهِۦ وَجَعَلَ عَلَيٰ بَصَرِهِۦ غِشَٰوَةٗ فَمَن يَهْدِيهِ مِنۢ بَعْدِ ٱللَّهِ
أَفَلَا تَذَّكَّرُونَ ﴿22﴾ وَقَالُواْ مَا هِيَ إِلَّا حَيَاتُنَا ٱلدُّنْيَا نَمُوتُ وَنَحْيَا
وَمَا يُهْلِكُنَا إِلَّا ٱلدَّهْرُ وَمَا لَهُم بِذَٰلِكَ مِنْ عِلْمٍ إِنْ هُمْ إِلَّا يَظُنُّونَ ﴿23﴾ وَإِذَا تُتْلَيٰ
عَلَيْهِمُۥٓ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٖ مَّا كَانَ حُجَّتَهُمْ إِلَّا أَن قَالُواْ ٱئْتُواْ بِـَٔابَآئِنَا إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿24﴾

16. Mun basu hujjoji mabayyana na daga al'amarin (addini na halak da haram da aiko Annabi SallAllahu alaihi wa sallama) basu saɓa cikin aiko shi basai bayan ilimi yazo musu, don zalinci a tsakaninsu (don hassada a gareshi), haƙiƙa Ubangiji yana hu-kunci a tsakaninsu ranar alƙiyama cikin abinda suka ka-sance suna sabani a cikinsa.
17. Sannan muka sanyaka (Ya An-nabi Sallallahu alaika wa salla-ma) cikin shari'a, sai kabi ta, kada kabi waɗanda basu da ili-mi (cikin bautar wanin Allah).
18. Su bazasu wadatar da komai ga buranka ba, (na daga Azabar Allah), haƙiƙa su azzalumai (wato kafirai) ba'alinsu majibinci ne ga ba'ali Allah Shine majibincin masu jin tsoronsa.
19. Wannan Alƙur'ani hujjoji ne ga mutane (dasuke lura da ita cikin hukunce-hukuncen da had-dodi), shiriya ne shi da rahama ga mutanen dasuke sakankan-cewa (da tashin alƙiyama).
20. Shin yanzu waɗannan da suka dashi miyagun aiyuka (kafirci da sabo) ma sanya su kamar waɗanda suka bada gaskiya sukayi ayyuka nagargaru rayu-warsu ta zama daidai, (wato ma'ana suna zaton ma sa su a lahira cikin alheri kamar mumi-nai, a cikin yalwar abinci daidai da rayuwarsu cikin duniya yay-in da sukace da muminai. "Wallahi in mun tashi muna da alheri irin wanda aka baku. Sai Ubangiji ya faɗa daidai da inka-rinsu), abinda suke hukunci dashiya mugusta, (al'amarin ba haka yake ba, su a lahira suna cikin azabasabanin rayuwarsa a duniya, muminai kuma a lahira suna cikin sakamako, saboda cikin su nagari a duniya).
21. Allah ya halicci sammai da gaskiya don kuma a sakawa kow-ace kai abindata aikata (na daga sabo da da'a, kafirai bazaiyi daidai da mumini ba). Su baza a zalince su ba.

(SHASHIN SAIYFO'INSU DA SAKAMAKONSU A KANTA RANAR ALƘIYAMA)

22. Bani labarin wanda ya riki Ubangijinsa son zuciyarsa (wato abinda yake son sa na dutse bayan wani dutsen yagan shi yafi shi kyau), Allah ya ɓatar dashi bisa ilimi daga Allah (wato Allah yasan cewa shi batacce ne tun kafin ya halicce shi) ya yimke bisa idanuwansa da kunnensa (bai ji shiriyaba bai hankalta ba) ya rufe idonsa (na zuci bai ga shiriya ba, to yanzu wannan ya shiriya? Jawa-bi A'a). To wa zai shirye shi ba Allah ba? (Wato tun da Allah ya ɓatar dashi ba mai shiriyarsa) Shin to ba kwa wa'azantu ba? (1).
23. Masu musun tashin Alƙiyama sukace "Ba wata rayuwa sai rayuwarmu ta duniya, mu mutu mu rayu (wadansu su mutu wadansu su rayu, wato takan haife-haife) ba abinda yake hal-akar da mu sai yau da kullum. (Ubangiji ta'ala yace), "Basu da wani da wannan canenka (magana), su basu kasance basai suna zato kawai.
24. Idan ana karatawan ayoyinmu a garesu (alƙur'ani mai shiryarwa a kan ikon mu a kan tashin alƙiyama) halin kasancewa ayoyin mabayyana, ba wani abu daya kasance hujjarsu, sai kaw-ai sukace, "Kuzo mana da iyayenmu (wato ku raya mana su) inkun kasance magasgata (da cewa za a tashe mu in mun mutu).

1) Na daga dutse da waninsa kamar rana da wata. na daga abin bautawa ba Allah ba. mai hankali ne ko wanin mai hankali. Kafirci dai Shine bauta ga wanin Allah, wato a nemi a kusania izuwa wanin Allah da bauta. kamar da alce neman kusanta izuwa Allah. wannan Shine kafirci. Amma ziyarar Salihai da An-nabawa to baya daga cikin bauta garesu. bari, ita dai tana daga babin musabbabiya cikin anfanin wani domin neman yardarwa ga waliyai. da salati da salami ga Annabawa, addu'a ne ga wani da wannan. ba shakka cewa wannan muium da aka nema Allah ya yarda dashi ko kara isira da aminci. wanda aka yiwa wannan zai amfanu da, ita. wanda yayi musabbabiyan nan kuma Shine wanda yayi addu'ar ko yayi salatin shima zai anfa-nu, saboda a hadisi Annabi Sallallahu alaihi wa sallama yace, "kai ma kana da kamar wannan. al'amarin". yakoma cewa ziyara ta salihai da tawassuli dasu yana daga da'ar Allah, ma'abocinta kuma abin so ne gurin Ubangiji domin mafi soyuwar bayin Allah izuwa Allah wanda yafi su anfani ga bayin-sa, maganar Ubangiji dayace suna sada abinda Ubangiji yayi umarni a sadashi, to basaɓo bane balle ta zama shirka kamar yadda ma'abota jahilci murakkabi suka kudure shi, ma'abota akida karkatacciya. -Sawi-

قُلِ اللَّهُ يُحْيِيكُمْ ثُمَّ يُمِيتُكُمْ ثُمَّ يَجْمَعُكُمْ إِلَىٰ يَوْمِ الْقِيَامَةِ لَا رَيْبَ فِيهِ
وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ النَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿25﴾ وَلِلَّهِ مُلْكُ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ
وَيَوْمَ تَقُومُ السَّاعَةُ يَوْمَئِذٍ يَخْسَرُ الْمُبْطِلُونَ ﴿26﴾ وَتَرَىٰ كُلَّ أُمَّةٍ جَاثِيَةً
كُلُّ أُمَّةٍ تُدْعَىٰ إِلَىٰ كِتَابِهَا الْيَوْمَ تُجْزَوْنَ مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿27﴾
هَٰذَا كِتَابُنَا يَنطِقُ عَلَيْكُم بِالْحَقِّ إِنَّا كُنَّا نَسْتَنسِخُ مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿28﴾
فَأَمَّا الَّذِينَ آمَنُوا وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ فَيُدْخِلُهُمْ رَبُّهُمْ فِي رَحْمَتِهِ ذَٰلِكَ
هُوَ الْفَوْزُ الْمُبِينُ ﴿29﴾ وَأَمَّا الَّذِينَ كَفَرُوا أَفَلَمْ تَكُنْ آيَاتِي تُتْلَىٰ عَلَيْكُمْ
فَاسْتَكْبَرْتُمْ وَكُنتُمْ قَوْمًا مُّجْرِمِينَ ﴿30﴾ وَإِذَا قِيلَ إِنَّ وَعْدَ اللَّهِ حَقٌّ
وَالسَّاعَةُ لَا رَيْبَ فِيهَا قُلْتُم مَّا نَدْرِي مَا السَّاعَةُ إِن نَّظُنُّ إِلَّا ظَنًّا
وَمَا نَحْنُ بِمُسْتَيْقِنِينَ ﴿31﴾ وَبَدَا لَهُمْ سَيِّئَاتُ مَا عَمِلُوا وَحَاقَ بِهِم
مَّا كَانُوا بِهِ يَسْتَهْزِئُونَ ﴿32﴾ وَقِيلَ الْيَوْمَ نَنسَاكُمْ كَمَا نَسِيتُمْ لِقَاءَ يَوْمِكُمْ هَٰذَا
وَمَأْوَاكُمُ النَّارُ وَمَا لَكُم مِّن نَّاصِرِينَ ﴿33﴾ ذَٰلِكُم بِأَنَّكُمُ اتَّخَذْتُمْ آيَاتِ اللَّهِ
هُزُؤًا وَغَرَّتْكُمُ الْحَيَاةُ الدُّنْيَا فَالْيَوْمَ لَا يَخْرُجُونَ مِنْهَا وَلَا هُمْ يُسْتَعْتَبُونَ ﴿34﴾
فَلِلَّهِ الْحَمْدُ رَبِّ السَّمَاوَاتِ وَرَبِّ الْأَرْضِ رَبِّ الْعَالَمِينَ ﴿35﴾
وَلَهُ الْكِبْرِيَاءُ فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ وَهُوَ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ ﴿36﴾

(RADDI A KAN DUHURRIYAWA DA RASHA DA MAKAMANTANSU)

25. Cene, (dasu) Allah ne mai raya-ku (zamanin da kuka kasance digon maniyi), sannan ya karɓi ranku, sannan ya tara ku (kuna rayayyu), izuwa ranar alƙiyama ba kokwanto a cikinsa, saidai yawancin mutane (sune masu faɗar wannan magana da maka-mantansu) basu san (haka) ba.
26. Mulkin sammai da ƙassai yana gurin Ubangiji, ranar da alƙiyama take tashi, a wannan rana kafirai tabewarsu zata bayyana, (wato su faɗa wuta).
27. Kana ganin kowace al'umma (masu addini) tana durkushe (a kan gwiwatata) kowace al'umma ana kiranta izuwa litta-fin aikinta, a yau ake saka muku sakamakon abinda kuka ka-sance kuna aikatawa.
28. Wannan littafinmu ne, (wato lit-tafin Mala'iku masu gadin bayi), yana furuci a kankuda gaskiya, haƙiƙa mu mun tabbata muna rubuce abinda kuka ka-sance kuna aikatawa (don ayi muku sakamakonsa).
29. Amma waɗanda suka na da gaskiya sukayi aiki nagargaru to ubangijinsu zai shigar dasu cikin aljannarsa, waneanenka Shine rabo mai girma.
30. Amma waɗanda suka kafirta (za a ce dasu), "Shin to ayoyina (Alƙur'ani bata kasance ana ka-ranta ta gareku ba amma kukayi girman kai, kuma kuka zamo mutane masu mugun laifi (kafi-rai?).
31. Idan akace daku ,(yaku waɗannan kafurai) " Haƙiƙa al-kawarin Allah (na tashin Alƙiyama) gaskiya ne, kuma sa'ar tashin alƙiyama ba kokon-to a cikinta", Sai kukan ce, "bamu san Menene sa'ar tashin al-kiyama ba, (Mu) Barna zaton (komai game da ita), sai zato (mai rauni), kuma mu ba masu sakankancewa bane (da zuwan-ta).
32. Sai miyagun abubuwan da suka aikata (a duniya) suka baiyana garesu (a lahira), kuma abinda suka kasance suna yin isgiki dashi (na azaba) ya sauka garesu.
33. Sai a ce (dasu), "a yau zamu manta ku (wato zamu barku a cikin wuta) kamar yadda kuka manta gamuwa dayininku wan-nan (wato kuka bar aikin alheri don gamuwa dashi), makomar ku wuta, kuma bakuda masu taimako (da zasu tsare ku daga gareta).
34. "Wancanenku ya kasance ne sa-boda cewa ku kun riRi ayoyin Allah (Alƙur'ani) ababan yiwa izgili, kuma rayuwar duniya ta rude ku (har kuka ce, "babu alƙiyama ba hisabi) to a yau baza a fitar dasu daga cikin wuta ba, kuma baza a nemi yardarwa daga garesu ba, (wato baza a nema su yardar da Allah bada tubada biyayya domin a rannan bazasuyianfani ba).
35. To dukkan yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin sammai, kuma Ubangijin ƙassai, Ubangijin ta-likai.
36. Kuma ƙasaitar girma ya tabbata ga Allah a cikin sammai da ƙassai, kuma Shine mabuwayi, gwani.

46 سُورَةُ الأحقاف مَكِّيَّة
وَهِيَ أَرْبَعٌ وَثَلَاثُونَ ءَايَةً 34

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

حزب

* حمٓ تَنزِيلُ الْكِتَٰبِ مِنَ اللَّهِ الْعَزِيزِ الْحَكِيمِ ﴿1﴾ مَا خَلَقْنَا السَّمَٰوَٰتِ
وَالْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا إِلَّا بِالْحَقِّ وَأَجَلٍ مُّسَمًّى وَالَّذِينَ كَفَرُوا عَمَّا أُنذِرُوا
مُعْرِضُونَ ﴿2﴾ قُلْ أَرَٰيْتُم مَّا تَدْعُونَ مِن دُونِ اللَّهِ أَرُونِيَ مَاذَا خَلَقُوا
مِنَ الْأَرْضِ أَمْ لَهُمْ شِرْكٌ فِي السَّمَٰوَٰتِ ائْتُونِي بِكِتَٰبٍ مِّن قَبْلِ هَٰذَا
أَوْ أَثَٰرَةٍ مِّنْ عِلْمٍ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿3﴾ وَمَنْ أَضَلُّ مِمَّن يَدْعُوا مِن دُونِ اللَّهِ
مَن لَّا يَسْتَجِيبُ لَهُ إِلَىٰ يَوْمِ الْقِيَٰمَةِ وَهُمْ عَن دُعَآئِهِمْ غَٰفِلُونَ ﴿4﴾
وَإِذَا حُشِرَ النَّاسُ كَانُوا لَهُمْ أَعْدَآءً وَكَانُوا بِعِبَادَتِهِمْ كَٰفِرِينَ ﴿5﴾ وَإِذَا تُتْلَىٰ
عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٍ قَالَ الَّذِينَ كَفَرُوا لِلْحَقِّ لَمَّا جَآءَهُمْ هَٰذَا سِحْرٌ مُّبِينٌ ﴿6﴾
أَمْ يَقُولُونَ افْتَرَىٰهُ قُلْ إِنِ افْتَرَيْتُهُ فَلَا تَمْلِكُونَ لِي مِنَ اللَّهِ شَيْـًٔا
هُوَ أَعْلَمُ بِمَا تُفِيضُونَ فِيهِ كَفَىٰ بِهِ شَهِيدًا بَيْنِي وَبَيْنَكُمْ وَهُوَ الْغَفُورُ الرَّحِيمُ ﴿7﴾
قُلْ مَا كُنتُ بِدْعًا مِّنَ الرُّسُلِ وَمَا أَدْرِي مَا يُفْعَلُ بِي وَلَا بِكُمْ
إِنْ أَتَّبِعُ إِلَّا مَا يُوحَىٰ إِلَيَّ وَمَا أَنَا إِلَّا نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿8﴾

Wannan Sura Itace Suratul LAHAKAFI
A Makka Aka Saukar Da Ita Aya Talatin Da HUDU Ce (34)
hia farawa dasunan Ubangiji Mai Jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan sura ta tattara a kan tauhi-di da tabbatar da Annabci da gaskiyar Annabi Sallallahu Alaihi Wasallama a cikin dukkan abinda yayi da'awa da rad-din rikici-rikicensu a cikin Alƙur'ani da Annabci da rarrashin Annabi Sallallahu Alaihi Wasal-lama da bayanin matsayin 'ya'ya daga iyayensu da sanya misalce-misalce ga mushurkai da mutanen Adu da waninsu da bayanin jawuwar aljannu gareshi, waɗanda ba a ganinsu, donya nutsu sallallahu alaihi wasal-lama da tabbatar da tashin al-kiyama; an cika surar da nasiha mai tsada ga Annabi sallallahu alaihi wasallama da dukkan wanda ya tsaya da kira izuwa Allah wato hasali dai wannan sura ta tabbatar da samuwar Allah, da Annabcin manzon Allah sallallahu alaihi wasallama da bata shurka da tabbatar da An-nabci da lahira).

1. (Allahu a'almu bimuradihi biza-lika) saukar wannan alƙur'ani daga Allah ne mabuwayi gwani.
2. Bamu halicci sammai da ƙassaida abinda yake tsakaninsu basaida gaskiya, (donya shtryar bisa ikonmu da kadaitakarmu) izuwa ajali abin anbato (izuwa ranar alƙiyama) waɗanda suka kafirta masu bijire wa ne da abinda aka basu tsoro dashi (na azaba).
3. Cene "ku bani labarin abinda kuke bautawa ba Allah ba (gu-maka,) ku bani labarin abinda suka halittashine ƙasa, shin suna da tarayya ne cikin halittar sammai (tareda Allah ko babu)? Kuzo mini da littafi (abin saukarwa) daga) gaban wannan (alƙur'ani) ko wani dan diddigar ilimi da ake ruwaitowa ga mutanen farko (a kan ingan-cin zancenku a cikin da'awar ku ga bautar gumaka cewa tana ku-santa ku izuwa Allah) inkun kasance magasgata (cikin da'awarku).
4. Ba (faya mafi Bacewa daga wan-da yake bautawa wanda bazai amsa masa ba izuwa ranar alƙiyama ba Allah ba. (Sune gumaka, bazasu amfanawa mai bauta musu ba izuwa wani abu da aka tambayesu har abada.) Su marafkana ne ga buran bau-tar dasuke musu, (domin cewa sandaran-u ne basu da hankali.)
5. Idan an tara mutane kumakan nan zasu kasance magauta ga masu bauta a garesu, su kuma masu bautar zasu kasance masu musu ga bautar dasuke musu.

(RIKICE-RIKICENSU GA AIKEN ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAMA DA GASKIYAR ALƘUR'ANI)

6. Idan ana karanta ayayinmu Shine Alƙur'ani a garesu (mutanen Makka) halin kasancewarta ma-bayyani; waɗanda suka kafirce wa gaskiya Shine Alƙur'ani yayin dayazo musu sai sukace wannan tsafi ne mabayyani.
7. Bari! suna cewa "Kirkirar Alƙur'ani yayi." Cene in kurkirar-sa nayi (takdiri) to bazaku mallaki wani abu nawa (daga Allah) ba, (wato bazaku iya ije azabar ga burana ba in Allah zai mini azabar;) Shine masani da abinda kuke kutsawa wato kuke faɗa a cikin Alƙur'ani) ya isa shaida tsakanina da ku, Shine mai gafara (ga wanda ya tuba) mai jin kai (gareshi saboda haka bai gaggauta masu da azaba ba.)
8. Cene "Ni ban kasance farau daga cikin manzanni ba (wato ban kasance farkon ma'aiki ba, da yawa waɗanda suka wuce gaba-na, yaya zaku karyatani?) Ban san abinda ake aikatawa dani daku ,ba, (za a fid danine daga garina ko za a kashe ni kamar yadda aka aikata ga annabawan da ke gabana, ko zaku jejjefe ni da duwatsu, ko za a kisife ƙasa da ku? Ni bana bin komai face abinda ake aikowa gare ni, ni ban kasance ba face mai gargaɗi ma mabaiyanin gargaɗi ".

قُلْ أَرَآيْتُمُۥٓ إِن كَانَ مِنْ عِندِ اِ۬للَّهِ وَكَفَرْتُم بِهِۦ وَشَهِدَ شَاهِدٞ
مِّنۢ بَنِےٓ إِسْرَآءِيلَ عَلَيٰ مِثْلِهِۦ فَـَٔامَنَ وَاسْتَكْبَرْتُمُۥٓۖ إِنَّ اَ۬للَّهَ لَا يَهْدِے اِ۬لْقَوْمَ
اَ۬لظَّٰلِمِينَۖ ۝9 وَقَالَ اَ۬لذِينَ كَفَرُواْ لِلذِينَ ءَامَنُواْ لَوْ كَانَ خَيْراٗ مَّا سَبَقُونَآ
إِلَيْهِۖ وَإِذْ لَمْ يَهْتَدُواْ بِهِۦ فَسَيَقُولُونَ هَٰذَآ إِفْكٞ قَدِيمٞۖ ۝10 وَمِن قَبْلِهِۦ
كِتَٰبُ مُوسَيٰٓ إِمَاماٗ وَرَحْمَةٗۖ وَهَٰذَا كِتَٰبٞ مُّصَدِّقٞ لِّسَاناً عَرَبِيّاٗ
لِّتُنذِرَ اَ۬لذِينَ ظَلَمُواْ وَبُشْرَيٰ لِلْمُحْسِنِينَۖ ۝11 إِنَّ اَ۬لذِينَ قَالُواْ رَبُّنَا اَ۬للَّهُ
ثُمَّ اَ۪سْتَقَٰمُواْ فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَۖ ۝12 أُوْلَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ
اُ۬لْجَنَّةِ خَٰلِدِينَ فِيهَا جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ يَعْمَلُونَۖ ۝13 * وَوَصَّيْنَا ثمن
اَ۬لْإِنسَٰنَ بِوَٰلِدَيْهِ حُسْناًۖ حَمَلَتْهُ أُمُّهُۥ كُرْهاٗ وَوَضَعَتْهُ كُرْهاٗ
وَحَمْلُهُۥ وَفِصَٰلُهُۥ ثَلَٰثُونَ شَهْراًۖ حَتَّيٰٓ إِذَا بَلَغَ أَشُدَّهُۥ وَبَلَغَ
أَرْبَعِينَ سَنَةٗ قَالَ رَبِّ أَوْزِعْنِيَ أَنْ أَشْكُرَ نِعْمَتَكَ
اَ۬لتِے أَنْعَمْتَ عَلَيَّ وَعَلَيٰ وَٰلِدَيَّ وَأَنَ اَعْمَلَ صَٰلِحاٗ تَرْضَيٰهُ
وَأَصْلِحْ لِے فِے ذُرِّيَّتِيَ إِنِّے تُبْتُ إِلَيْكَ وَإِنِّے مِنَ اَ۬لْمُسْلِمِينَۖ ۝14
أُوْلَٰٓئِكَ اَ۬لذِينَ يُتَقَبَّلُ عَنْهُمْ أَحْسَنُ مَا عَمِلُواْ وَيُتَجَاوَزُ
عَن سَيِّـَٔاتِهِمْ فِےٓ أَصْحَٰبِ اِ۬لْجَنَّةِۖ وَعْدَ اَ۬لصِّدْقِ اِ۬لذِے كَانُواْ يُوعَدُونَۖ ۝15

9. Cene "ku bani labarin Menene halinku) in alƙur'ani ya kasance daga gurin Allah; kuka kafirta dashi, mai shaidarwa ya shaidar bisa misalinsa ya bada gaskıyakukayi girman kai ga buran imani (sa'inbaku kasance azza-lumai ba?) Haƙiƙa Ubangiji baya shiriyar mutane azzalumai."
10. Waɗanda suka kafirta sukace ga waɗanda suka bada gaskiya "Da imani ya kasance alheri da bazasu rigaye mu izuwa gare-shi ba" tun da basu shiriya dashi wannan Al£ur'ani ba, da sannu zasu ce "Wannan (Alƙur'ani) karyace dadaddiya."
11. Gaban Alƙur'ani akwai littafi Attaura, wannan Alƙur'ani mai gasgatawa ne, harshe Balarabe domin ya tsoratar da waɗanda sukayi zalinci (mutanen Mak-ka,) kuma shi albishir ne ga ma-sana Allah.
12. Haka waɗanda sukace su a kan da'ar Allah suke, to ba tsoro garesu a kan abinda zasu gabata a lahira,) bazasuyibakin ciki ba (a kan abinda suka bari a bayansu na iyalansu.)
13. WacTancananka sune 'yan aljan-na masu dawwama a cikinta, ana saka musu abinda suka ka-sance suna aikatawa' sakawa.

(BIN ALLAH TA'ALA DA BIN IYAYE DA FALALAR SAIYIDINA ABUBAKAR SIDDIḰU ALLAH YA KARA MASA YARDA)

14. Munyi wa mutum wasiya ta kyautatawa mahaifinsa, mahai-fiyarsa. Tayi cikinsa a cikin wahala, ta haife shi a cikin wa-hala, cikinsa dayaye shi (daga shan non) wata talatin (watashi-da mafi ƙarancin muddar ciki, sauran kuma sune mafi yawan muddar yaye, Ance in tayi ciki dashi watashida ko tara ta shayad dashi ragowar) har lok-acin daya isa mafi tsananinsa (wato mafi karfinsa, hankali da ra'ayi, wato mafi Karancinsa tal-atin da uku ko talatin) ya isa shekara arab'in (Shine aksarin mafi ƙarfi) sai yace da mahai-finsa Ubangijina (har izuwa ƙarshen ayar. Ta sauka a cikin Sayyidina Abubakar Siddiƙu zamanin daya cika shekara 40 bayan shekara 2 da aiko Annabi sallallahu alaihi wasallama saiya bada gaskiya da Annabi sal-lallahu alaihi wasallama sannan iyayensa suka bada gaskiyasannan dansa Abduirahamam, sannan jikansa Abu Atikin dan Adbun-ahamani sunansa Mu-hammadu, lakabinsa Abu Atikin dan Abdurrahamani jikan Sayy-idina Abubakar) ka kimsa mini in godewa ni'imarka wacce ka ni'imta gare m da mahaifina (Itace tauhidi) kuma ka kimsa mini in yi aiki na gari wanda zaka yarda dashi (ya'yanta mutum tara waɗanda suke muminai da ake musu azaba Don sun , musu-lunta) ka sa salaha mai natsuwa a cikin zumyata, (saboda haka duk zurriyassa muminai ne) haƙiƙa ni na tuba izuwa gareka haƙiƙa ni ina daga cikin masu rmKuwa izuwa gareka, haƙiƙa ni ina daga cikin musulmi.
15. Waɗancananka (masu waɗannan magana Abubakar da waninsa) sune waɗanda ake karbar kyak-kyawan abinda suka aikata, rangwame ga miyagun ayyukansu a cikin 'yan aljanna; alƙawarin gaskiya wanda suka kasance anayi musu alƙawari (dashi).

وَالَّذِي قَالَ لِوَالِدَيْهِ أُفٍّ لَّكُمَا أَتَعِدَانِنِي أَنْ أُخْرَجَ وَقَدْ خَلَتِ الْقُرُونُ
مِن قَبْلِي وَهُمَا يَسْتَغِيثَانِ اللَّهَ وَيْلَكَ آمِنْ إِنَّ وَعْدَ اللَّهِ حَقٌّ
فَيَقُولُ مَا هَٰذَا إِلَّا أَسَاطِيرُ الْأَوَّلِينَ ﴿16﴾ أُولَٰئِكَ الَّذِينَ حَقَّ عَلَيْهِمُ الْقَوْلُ
فِي أُمَمٍ قَدْ خَلَتْ مِن قَبْلِهِم مِّنَ الْجِنِّ وَالْإِنسِ إِنَّهُمْ كَانُوا خَاسِرِينَ ﴿17﴾
وَلِكُلٍّ دَرَجَاتٌ مِّمَّا عَمِلُوا وَلِنُوَفِّيَهُمْ أَعْمَالَهُمْ وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿18﴾
وَيَوْمَ يُعْرَضُ الَّذِينَ كَفَرُوا عَلَى النَّارِ أَذْهَبْتُمْ طَيِّبَاتِكُمْ فِي حَيَاتِكُمُ الدُّنْيَا
وَاسْتَمْتَعْتُم بِهَا فَالْيَوْمَ تُجْزَوْنَ عَذَابَ الْهُونِ بِمَا كُنتُمْ تَسْتَكْبِرُونَ
فِي الْأَرْضِ بِغَيْرِ الْحَقِّ وَبِمَا كُنتُمْ تَفْسُقُونَ ﴿19﴾ * وَاذْكُرْ أَخَا عَادٍ
إِذْ أَنذَرَ قَوْمَهُ بِالْأَحْقَافِ وَقَدْ خَلَتِ النُّذُرُ مِن بَيْنِ يَدَيْهِ وَمِنْ خَلْفِهِ
أَلَّا تَعْبُدُوا إِلَّا اللَّهَ إِنِّي أَخَافُ عَلَيْكُمْ عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿20﴾ قَالُوا
أَجِئْتَنَا لِتَأْفِكَنَا عَنْ آلِهَتِنَا فَأْتِنَا بِمَا تَعِدُنَا إِن كُنتَ
مِنَ الصَّادِقِينَ ﴿21﴾ قَالَ إِنَّمَا الْعِلْمُ عِندَ اللَّهِ وَأُبَلِّغُكُم مَّا أُرْسِلْتُ بِهِ وَلَٰكِنِّيَ أَرَاكُمْ
قَوْمًا تَجْهَلُونَ ﴿22﴾ فَلَمَّا رَأَوْهُ عَارِضًا مُّسْتَقْبِلَ أَوْدِيَتِهِمْ قَالُوا هَٰذَا عَارِضٌ مُّمْطِرُنَا
بَلْ هُوَ مَا اسْتَعْجَلْتُم بِهِ رِيحٌ فِيهَا عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿23﴾ تُدَمِّرُ كُلَّ شَيْءٍ بِأَمْرِ رَبِّهَا
فَأَصْبَحُوا لَا تَرَىٰ إِلَّا مَسَاكِنُهُمْ كَذَٰلِكَ نَجْزِي الْقَوْمَ الْمُجْرِمِينَ ﴿24﴾

ربع

16. Wađanda sukace ga mahaifansu «tur da ku, kwa dinga tsorata ni a fid dani (daga kabari) alhali tsareku gabana sun wuce (basu fito daga kabari ba)» alhali su iyayen suna neman taimako da Allah, (a kan komowar dansu, dashiriyar dansu) «in baka komo bakaito ya tabbata gareka, ka bada gaskiya da tashin alƙiyama gaskiya ne», yace «wannan magana ta tashin Alƙiyama bai kasance ba si ƙaryace--ƙaryacen mutanen far-ko».
17. Wađancananka sune wađanda magana ta azabata tabbata a kansu, a cikin al'ummatai da suka shude gabansu na aljanu da mutane, haƙiƙa sun kasance taɓaɓɓu.
18. Darajoji sun tabbata ga kowane, (da mumini da kafiri, darajojin muminai a cikin aljanna madaukaka ne, darajojin kafirai a wuta maƙasƙanta ne) daga abinda suka aikata (na da'a, ko sabo) lallai Ubangiji zai saka musu da abinda suka aikata, su baza a zalince su komai ba, (da tauye mumini da karawa ga ka-firi).
19. Ranar da ake bijirar da wađanda suka kafirta bisa wuta (Shine a yayeta garesu a ce dasu) "kun tafiyad da dadadenku a cikin rayuwarku ta duniya kun ni'imtu da ita, to a yau za a sake muku azabar wulakanci saboda kasancewarku kuna girman kai cikin ƙasa, bada gaskiya ba, kuma kuna fasikanci. (Za ayi musu azabasaboda wannan).

(ƘISSAR ANNABI HUDU TAREDA MUTANENSA ADU)

20. Ka ambaci dan uwan Adu (An-nabi Hudu alaihissalamu) zama-nin daya tsoratar da mutanensa a Lahakafu (zaza ne a ƙasar Ya-men). Alhali manzanni sun wuce nan gaba gareshi da kuma bayansa izuwa mutanensa yace dasu; "Ka daku ,bautawa kowa sai Allah, ni ina jin tsoron aza bar rana mai girma gareku inkun bautawa wanin Allah.
21. Sukace "kazo mana donka juyad da mu ga buran bautar iy-ayen gijinmu? Kazo mana da abinda kake alKawari dashi (na azaba a kan bautarta) in ka ka-sance cikin magasgata (cewa azabaza tazo mana". Annabi Hudu yace).
22. "Dahir dai ilimi yana gurin Allah Shine yasan sandaza tazo muku; ni na iyar muku abinda aka aiko ni dashi izuwa gareku saidai ni ina ganin ku mutane ne kuda kuke aikin jahilci."
23. Yayin da suka ga azaban nan ta girgije (wato hadari) ya gindaya a sassan sama yagabato sosai a kansu, sai sukace "Wannan ha-diri ne mai mana ruwa". Sai Ubangiji yace "Bari! Shine abinda kuke gaggawansa" iskace wacce azaba mai rađađi take cikinta.
24. Tana halakar da kowane abu da izinin Ubangijinta (saita halakar da mazansu da matansu da kananansu da manyansu, Shine tayi sama ta kyakketa su da kayansu suka halaka baki đaya, Annabi Hudu ya ragu da wanda ya bada gaskiya su 4.000) sai suka wayi gari basa ganin ko-mai sai guraren zamansu, tamk-ar da muka saka musu muke sa-kawa mutane ma'abota laifi.

وَلَقَدْ مَكَّنَّٰهُمْ فِيمَآ إِن مَّكَّنَّٰكُمْ فِيهِ وَجَعَلْنَا لَهُمْ سَمْعاً وَأَبْصَٰراً
وَأَفْـِٔدَةً فَمَآ أَغْنَىٰ عَنْهُمْ سَمْعُهُمْ وَلَآ أَبْصَٰرُهُمْ وَلَآ أَفْـِٔدَتُهُم مِّن شَيْءٍ
إِذْ كَانُواْ يَجْحَدُونَ بِـَٔايَٰتِ اِ۬للَّهِ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿25﴾
وَلَقَدْ أَهْلَكْنَا مَا حَوْلَكُم مِّنَ اَ۬لْقُرَىٰ وَصَرَّفْنَا اَ۬لْأٓيَٰتِ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿26﴾
فَلَوْلَا نَصَرَهُمُ اُ۬لَّذِينَ اَ۪تَّخَذُواْ مِن دُونِ اِ۬للَّهِ قُرْبَاناً ـَٔالِهَةَۢ بَلْ ضَلُّواْ عَنْهُمْ
وَذَٰلِكَ إِفْكُهُمْ وَمَا كَانُواْ يَفْتَرُونَ ﴿27﴾ وَإِذْ صَرَفْنَا إِلَيْكَ نَفَراً
مِّنَ اَ۬لْجِنِّ يَسْتَمِعُونَ اَ۬لْقُرْءَانَ فَلَمَّا حَضَرُوهُ قَالُواْ أَنصِتُواْ فَلَمَّا قُضِيَ
وَلَّوْاْ إِلَىٰ قَوْمِهِم مُّنذِرِينَ ﴿28﴾ قَالُواْ يَٰقَوْمَنَا إِنَّا سَمِعْنَا كِتَٰباً اُنزِلَ مِنۢ بَعْدِ مُوسَىٰ
مُصَدِّقاً لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ يَهْدِيٓ إِلَى اَ۬لْحَقِّ وَإِلَىٰ طَرِيقٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿29﴾ يَٰقَوْمَنَا أَجِيبُواْ
دَاعِيَ اَ۬للَّهِ وَءَامِنُواْ بِهِۦ يَغْفِرْ لَكُم مِّن ذُنُوبِكُمْ وَيُجِرْكُم مِّنْ عَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿30﴾
وَمَن لَّا يُجِبْ دَاعِيَ اَ۬للَّهِ فَلَيْسَ بِمُعْجِزٍ فِي اِ۬لْأَرْضِ وَلَيْسَ لَهُۥ مِن دُونِهِۦٓ أَوْلِيَآءُ
أُوْلَٰٓئِكَ فِي ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿31﴾ * أَوَلَمْ يَرَوْاْ أَنَّ اَ۬للَّهَ اَ۬لَّذِي خَلَقَ اَ۬لسَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضَ ثمن
وَلَمْ يَعْيَ بِخَلْقِهِنَّ بِقَٰدِرٍ عَلَىٰٓ أَن يُحْـِۧيَ اَ۬لْمَوْتَىٰ بَلَىٰٓ إِنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ
قَدِيرٌ ﴿32﴾ وَيَوْمَ يُعْرَضُ اُ۬لَّذِينَ كَفَرُواْ عَلَى اَ۬لنَّارِ أَلَيْسَ هَٰذَا بِالْحَقِّ
قَالُواْ بَلَىٰ وَرَبِّنَا قَالَ فَذُوقُواْ اُ۬لْعَذَابَ بِمَا كُنتُمْ تَكْفُرُونَ ﴿33﴾

25. Haƙiƙa mum kafa ikonku cikin abinda bamu kafawa mutanen Makka iko a cikinsa ba, (na Rarfi da dukiya) mun sanya musu kunnuwa da idon dubana zukata, kunnuwansu da idanun-su da zukatansu bata wadatar musu da komai ba, Don sun , ka-sance suna musun ayoyin Allah, abinda suke izigili dashiya sauka garesu.
26. Haƙiƙa mun halakar da abinda yake daura daku ,na daga alkar-yatu, (kamar Samudu da Adu da mutanen Annabi Luɗu), mun sarrafa ayoyi wato hujjoji ma-baiyana donsu komo ga buran Kafirai.
27. Saboda me waɗanda suka riƙesu ubangiji ba Allah basuna kusanto dasu izuwa Allah, donme basu ije musu azaba ga bu-ransu, bari sun ɓace ga buran shiriyassu. Wancananka (riƙon gumaka iyayen giji ba Allah ba) Shine Karyassu da abinda suka kasance suna girbakarya.

[JINNU NASIBINA] KO NINAWA DA BADA GASKIYARSU GA MA'AIKI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA

28. Ka ambaci zamanin da muka karkato maka da jama'a na alja-nu izuwa gareka (sune aljannun Nasibina a Yamen ko kuma al-jannun Ninawa a Mausil, su bakwai ne ko takwas wannan ya aukune lokacin da manzon Allah sallallahu alaihi wasallama yake yin sallah shi da Sahab-bansa) suna sauraron Alkur'am yayin da suka halarce shi sai ba'alin su yace da ba'ali «kuyi kawai (saboda sauraronsa)». Yayin da aka gama karantunsa, sai suka juya izuwa ba'ali suna basu tsoro da azaba in basu bada gaskiya ba. (Waɗannan Alja-nu kuwa sun kasance Yahudawa ne alhali sun musulunta).
29. Sai ku ce "yaku mutanenmu! haƙiƙa Munji littafi (wato Alƙur'ani) an saukad dashi bayan Annabi Musa, mai gasga-ta abinda ke gabansa, (kamar Attaura), yana shiryarwa izuwa tafarkin gaskiya; musulunci.
30. Ku amsa makirayin Allah (Shine ma'aikin Allah sallallahu alaihi wasallama mai kira izuwa imani) ku bada gaskiya dashi Allah ya gafarta maku daga zu-nubanku (domin akwai mazali-mu daga cikin zunuban ba a ga-fartata sai da yardar mutanenta). Zai tserar daku ,daga azaba mai raɗaɗi.
31. Duk wanda bai amsawa maki-rayin Allah ba, bazai tserewa Allah a cikin ƙasa ba, bashi da majibinta ba Allah ba. Wadancanenka suna cikin bata mabaiyani.

(DAGA DALILAN TASHIN ALƘIYAMA)

32. Shin (masu musun tashin alƙiyama) basu sani ba cewa Allah wanda ya halicci sammai da ƙassai alhali bai gajiva da halittarsu ba, mai ikone a kan raya matattu. haƙiƙa shi mai ikone bisa komai.
33. Ranar da ake bijirar da waɗanda suka kafirta kan wuta (Shine ayi musu azabada ita, a ce dasu,) "Shin wannan azabtawar nan ba gaskiya bane? Saisu ce «ai gaskiya ne; mun rantse da Ubangijinmu», sai yace "Ku ɗanɗani azabasaboda kasance-warku kafira."

فَاصْبِرْ كَمَا صَبَرَ أُوْلُواْ الْعَزْمِ مِنَ الرُّسُلِ وَلَا تَسْتَعْجِل
لَّهُمْ كَأَنَّهُمْ يَوْمَ يَرَوْنَ مَا يُوعَدُونَ لَمْ يَلْبَثُواْ إِلَّا سَاعَةً
مِّن نَّهَارٍ بَلَٰغٌ فَهَلْ يُهْلَكُ إِلَّا الْقَوْمُ الْفَٰسِقُونَ ﴿34﴾

47 سُورَةُ مُحَمَّدٍ ﷺ مَدَنِيَّةٌ
وَهِيَ تِسْعٌ وَثَلَاثُونَ ءَايَةً 39

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

الَّذِينَ كَفَرُواْ وَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ اللَّهِ أَضَلَّ أَعْمَٰلَهُمْ ﴿1﴾ وَالَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ
الصَّٰلِحَٰتِ وَءَامَنُواْ بِمَا نُزِّلَ عَلَىٰ مُحَمَّدٍ وَهُوَ الْحَقُّ مِن رَّبِّهِمْ كَفَّرَ عَنْهُمْ سَيِّـَٔاتِهِمْ
وَأَصْلَحَ بَالَهُمْ ﴿2﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّ الَّذِينَ كَفَرُواْ اتَّبَعُواْ الْبَٰطِلَ وَأَنَّ الَّذِينَ ءَامَنُواْ
اتَّبَعُواْ الْحَقَّ مِن رَّبِّهِمْ كَذَٰلِكَ يَضْرِبُ اللَّهُ لِلنَّاسِ أَمْثَٰلَهُمْ ﴿3﴾ فَإِذَا لَقِيتُمُ
الَّذِينَ كَفَرُواْ فَضَرْبَ الرِّقَابِ حَتَّىٰ إِذَا أَثْخَنتُمُوهُمْ فَشُدُّواْ الْوَثَاقَ
فَإِمَّا مَنًّا بَعْدُ وَإِمَّا فِدَاءً حَتَّىٰ تَضَعَ الْحَرْبُ أَوْزَارَهَا ﴿4﴾ ذَٰلِكَ وَلَوْ يَشَاءُ اللَّهُ
لَانتَصَرَ مِنْهُمْ وَلَٰكِن لِّيَبْلُوَاْ بَعْضَكُم بِبَعْضٍ وَالَّذِينَ قُتِلُواْ فِي سَبِيلِ اللَّهِ فَلَن يُضِلَّ
أَعْمَٰلَهُمْ ﴿5﴾ سَيَهْدِيهِمْ وَيُصْلِحُ بَالَهُمْ ﴿6﴾ وَيُدْخِلُهُمُ الْجَنَّةَ عَرَّفَهَا لَهُمْ ﴿7﴾ يَٰأَيُّهَا
الَّذِينَ ءَامَنُواْ إِن تَنصُرُواْ اللَّهَ يَنصُرْكُمْ وَيُثَبِّتْ أَقْدَامَكُمْ ﴿8﴾

(UMARNI DA HAKURI DAGA MANZANNI ALAIHIMUSSALAMU)

34. Kayi ha^uri bisa cutar mutanen-ka tamfar da ma'abota dauriya na daga manzanni sukayi (bisa tsanance-tsanance, kada kayi yi garaje garesu bisa saukar azaba garesu, zata sauka ne garesu, kai kace yayin da ake musu al-washi na azaba a lahira saboda tsawonsa basu zauna a cikin za-tonsu basai sau ɗaya ta wuni, wannan Alƙur'ani iyarwa ne daga Allah izuwa gareku. Ba a halakarwa yayin saukarwar aza-ban nan sai mutane fasikai (ka-firai).

Wannan Sura Itace Suratul KITALI

A Madina Aka. Saukar Da Ita Aya Talatin Da Tara Ce (39)

Ina Farawa Dasunan Ubangui Mai Jinkan Taukai A Duniya Gabadaya, Mai Jinkan Muminai ALAHKAA Keɓe

(WANNAN SURA TA TABBATAR BISA HALULUWAN KAFIRAI DA MUMINAI A DUNIYA DA LAHIRA DA KABALTAWA TSAKANINSU DA AMBATON HUKUNCE-HUKUNCEN YAKI)


1. Waɗanda suka kafirta (daga mu-tanen Makka) suka hana wanin-su bin hanyar Allah, (ga buran imani,) Allah yayi watsi da aiy-ukansu. (Kamar ciyad da abinci da sadar da zumunta, bazasu ga sakamakonta ba; za ayi musu samakako da ita ta babin falalar Ubangiji.
2. Waɗanda suka bada gaskiya (sune Ansaru da waninsu sukai aiki nagari suka bada gaskiya da abinda aka saukar ga Annabi Muhammadu (Sallallahu alaihi wasallama Shine Alƙur'ani) al-hali Shine gaskiya daga Ubangijinsu ya gafarta musu miya-gun aikinsu, ya kyautata aikinsu (saboda haka basa sabonsa).
3. Wancanenka (watsi da aiki, da gafarta miyagun aiyuka) saboda haldRa waɗanda suka kafirta sun bi shaiɗan, waɗanda suka bada gaskiya sun bi gaskiya Shine alƙur'ani daga Ubangijinsu, kamar irin wannan bayanine Allah yake baiyanawa mutane haluluwansu (wato kafiri Allah yana watsi da aikinsa, mumini Allah yana gafarta kuskurensa.)

(ALƘUR'ANI DA MAGANAR YAKI)

4. Idan kuka gamu da waɗanda suka kafirta, to ƙu doke wuyayinsu, (ma'ana ku kashe su, yayi bay-ani da doke wuya saboda marin-jayi a cikin kisa yakan kasance da doke wuyaye) har idan kuka ƙasa yawaita kisa a cikinsu, to ku daure su tamau, da ƙangi (wandaShine wasaku) imma kuyi baiwa garesu baiwa (ku sake su bada komai ba,) imma ku fanshesu (da dukiyako ribatattu musulmi, wato ku ce "ga naku ku bamu namu) har mayaƙa su ajiye kayan yaJci na makami da waninsa (Shine kafurai su mu-sulunta ko su shigo cikin alkaw-ari wato wannan Itace matuƙa ga kisan, ko kuma ribacewa.)
5. Haka lamarin yake, da Allah yana so daya ɗanɗana musu kudassu ba tare dayaƙi,ba, saidai ya umarce kuda wannan ne, domin ya jarrabi ba'alinku da ba'alinsu; (wanda aka kashe naku ya faɗa Aljanna; nasu kuma ya faɗa wuta), waɗanda aka kashe su cikin tafarkin Ubangiji (ta sauka ne a ranar Uhudu alhali kisa da raunuka sun yawaita a cikin musulmi), to Allah bazaiyi watsi da aikinsu ba.
6. Da sannu Ubangiji zai shiryesu (a duniya da lahira izuwa abindazai anfane su. Abindazai anfane su a lahira aiki nagari, wandazai anfane su a lahira al-janna da abinda yake cikinta. Saboda haka abindazai sabi lamarin Allah bazai afku badaga garesu, saboda Allah ya kiyaye su daga sabanni) ya gya-ra halinsu (a cikin duniya da lahira). Abinda yake cikin duniyakuma da gyaran hali ya tabbata ga wanda ba a kashe ba, an kun-she su a cikin kutilu don rinjay-arwa.
7. Zai shigar dasu Aljanna daya baiyanata garesu. (Zasu shiga izuwa gidaddajinsu na Aljanna da matayensu da magidantansu badajagoraba).

(KARFAFA GWIWAR MASU KIRA IZUWA ALLAH)

8. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya! inkun taimaki Allah (wato addinisa) zai taimake ku (kan magautanku) zai tabbatar da dugaduganku (a cikin fagen fama).

وَالذِينَ كَفَرُوا فَتَعْساً لَّهُمْ وَأَضَلَّ أَعْمَالَهُمْ ۝9 ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ

كَرِهُوا مَا أَنزَلَ اللَّهُ فَأَحْبَطَ أَعْمَالَهُمْ ۝10 * أَفَلَمْ يَسِيرُوا فِي الْأَرْضِ
فَيَنظُرُوا كَيْفَ كَانَ عَاقِبَةُ الذِينَ مِن قَبْلِهِمْ دَمَّرَ اللَّهُ عَلَيْهِمْ وَلِلْكَافِرِينَ
أَمْثَالُهَا ۝11 ذَٰلِكَ بِأَنَّ اللَّهَ مَوْلَى الذِينَ ءَامَنُوا وَأَنَّ الْكَافِرِينَ لَا مَوْلَىٰ لَهُمْ ۝12
إِنَّ اللَّهَ يُدْخِلُ الذِينَ ءَامَنُوا وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ جَنَّاتٍ تَجْرِي مِن تَحْتِهَا
الْأَنْهَارُ وَالذِينَ كَفَرُوا يَتَمَتَّعُونَ وَيَأْكُلُونَ كَمَا تَأْكُلُ الْأَنْعَامُ
وَالنَّارُ مَثْوًى لَّهُمْ ۝13 وَكَأَيِّن مِّن قَرْيَةٍ هِيَ أَشَدُّ قُوَّةً مِّن قَرْيَتِكَ
الَّتِي أَخْرَجَتْكَ أَهْلَكْنَاهُمْ فَلَا نَاصِرَ لَهُمْ ۝14 أَفَمَن كَانَ عَلَىٰ بَيِّنَةٍ
مِّن رَّبِّهِ كَمَن زُيِّنَ لَهُ سُوءُ عَمَلِهِ وَاتَّبَعُوا أَهْوَاءَهُمْ ۝15 مَّثَلُ الْجَنَّةِ
الَّتِي وُعِدَ الْمُتَّقُونَ فِيهَا أَنْهَارٌ مِّن مَّاءٍ غَيْرِ ءَاسِنٍ وَأَنْهَارٌ مِّن لَّبَنٍ
لَّمْ يَتَغَيَّرْ طَعْمُهُ وَأَنْهَارٌ مِّنْ خَمْرٍ لَّذَّةٍ لِّلشَّارِبِينَ وَأَنْهَارٌ مِّنْ عَسَلٍ مُّصَفًّى
وَلَهُمْ فِيهَا مِن كُلِّ الثَّمَرَاتِ وَمَغْفِرَةٌ مِّن رَّبِّهِمْ كَمَنْ هُوَ خَالِدٌ فِي النَّارِ
وَسُقُوا مَاءً حَمِيماً فَقَطَّعَ أَمْعَاءَهُمْ ۝16 وَمِنْهُم مَّنْ يَسْتَمِعُ إِلَيْكَ
حَتَّىٰ إِذَا خَرَجُوا مِنْ عِندِكَ قَالُوا لِلذِينَ أُوتُوا الْعِلْمَ مَاذَا قَالَ ءَانِفاً
أُوْلَٰئِكَ الذِينَ طَبَعَ اللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ وَاتَّبَعُوا أَهْوَاءَهُمْ ۝17

9. Wađanda suka kafirta (daga. mu-tanen Makkah da waninsu) to sun halaka kuma Allah yayi watsi da aiyukansu.
10. Wancananka halakar kuwa, sa-boda Haƙiƙa cewa su sun ƙi abinda Allah ya saukar (na Alƙur'ani wanda ya tattarar da taklifi, wato đbra murgun bauta), to saiya wargaza aiyukansu.

(MUMINAI DA KAFIRAI DA DUNIYA DA LAHIRA)

11. Shin basuyitafiya bane a cikin ∟asa, su dubasu ga yaya alƙiblar wađanda suke gabansu ta kasance? Ubangiji yayi dan-daƙa a kansu (ya halakad da kawukansu da dukiyoyinsu), irin wannan mummunan karshe ya tabbata ga kafirai.

(NI'IMA DA AZABA RANAR ALƘIYAMA)

12. Wannan (taimakon muminai da mutsitstsike kafirai) saboda haƙiƙa cewa Ubangiji Shine mataimakin wađanda suka bada gaskiya, haƙiƙa kafirai ba gali-hu garesu.
13. Haƙiƙa Ubangiji yana shigar da wađanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru aljannatai wacce ƙoramu suke gudana cikinta, wadandTa suka kafirta suna morewa a duniya, suna ci tamfar yadda dabbobi suke ci (ba abinda ya dame su sai cikin-su da farjojinsu, basa waiwaye izuwa Lahira), wuTace mako-marsu.
14. Da yawa mutanen alƙaryaitace tafi mafi tsananin ƙarfi daga alKaryarka, (wato mutanen Makka), wacce ta fitar da kai, Muka halakar dasu ba mai tai-mako garesu.
15. To shin wanda yake da hujja daga Ubangijinsa (sune mumi-nai) ya zama kamar wanda aka kawata wa mummunan aikinsa (yagan shi kyakkyawa? Sune kafiran Makka) sim bi soye soy-en zukatansu (a cikin bautar gu-maka, watb ba tankaceceniya tsakaninsu).

(NI'IMA DA AZABA RANAR ALƘIYAMA)

16. Wato sifar Aljanna wacce aka aUcawarta ta ga masu tsoron Allah, akwai ƙoramu a cikinta na ruwa garau ba majirkici ba, da ƙoramu na nono wanda danđaninsa bai jirkita ba, (sabanin nonon duniya saboda yafita daga cikin hantsa) da ƙoramu na giya mai dađi ga masu sha da ƙoramu na zuma tatacce, (sabanin zuman duniya saboda yana fita ne daga cikku-nan kudan zuma, kaki yana cudanya dashi da waninsu) dangogin dukkan itaciya na garesu a cikintada gafara daga Ubangiji Ubangijinsu shiya yarda garesu, tareda kyautay-awassa izuwa garesu da abinda aka ambata, (sabanin shugaban bayi a duniya tareda ihsanin da yake musu, yakan zama mai fu-shi a kansu) zai zama kamar wanda yake madawwami cikin wuta. Aka sha dasu ruwa mai zafi ya kyarketa kayan cikinsu (suka fito daga dubaransu).

(MUNAFUKAI DASHIRYAYYU)

17. Akwai daga kafirai wanda yake sauraranka (a hudubar Juma'a suna munafikai), har dai lokacin da suKafita daga gurinka, saisu ce ga wanda aka basu ilimi (ga malaman Sahabbai ibn Mas'udin da ibn Abbasin suna cikinsu raliyallahu anhuma don izgili da ba'a) "me ya fađa ne yanzu?" Wadancanenka sune wađanda Allah ya yumlce zuka-tansu da kafirci sun bi soye-soyen zukatansu.

وَالَّذِينَ اَهْتَدَوْاْ زَادَهُمْ هُدًى وَءَاتَيٰهُمْ تَقْوَيٰهُمْ ﴿18﴾ فَهَلْ يَنظُرُونَ
إِلَّا اَلسَّاعَةَ أَن تَأْتِيَهُم بَغْتَةً فَقَدْ جَآءَ أَشْرَاطُهَا فَأَنَّىٰ لَهُمْ إِذَا جَآءَتْهُمْ
ذِكْرَيٰهُمْ ﴿19﴾ فَاعْلَمْ أَنَّهُۥ لَا إِلَٰهَ إِلَّا اَللَّهُ وَاسْتَغْفِرْ لِذَنبِكَ وَلِلْمُؤْمِنِينَ وَالْمُؤْمِنَٰتِ
وَاللَّهُ يَعْلَمُ مُتَقَلَّبَكُمْ وَمَثْوَيٰكُمْ ﴿20﴾ ۞ وَيَقُولُ اُلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَوْلَا نُزِّلَتْ
سُورَةٌ فَإِذَا أُنزِلَتْ سُورَةٌ مُّحْكَمَةٌ وَذُكِرَ فِيهَا اَلْقِتَالُ رَأَيْتَ اَلَّذِينَ
فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٌ يَنظُرُونَ إِلَيْكَ نَظَرَ اَلْمَغْشِيِّ عَلَيْهِ مِنَ اَلْمَوْتِ فَأَوْلَىٰ
لَهُمْ ﴿21﴾ طَاعَةٌ وَقَوْلٌ مَّعْرُوفٌ فَإِذَا عَزَمَ اَلْأَمْرُ فَلَوْ صَدَقُواْ اُللَّهَ لَكَانَ
خَيْراً لَّهُمْ ﴿22﴾ فَهَلْ عَسِيتُمُۥ إِن تَوَلَّيْتُمُۥ أَن تُفْسِدُواْ فِي اِلْأَرْضِ وَتُقَطِّعُواْ
أَرْحَامَكُمْ ﴿23﴾ أُوْلَٰٓئِكَ اَلَّذِينَ لَعَنَهُمُ اُللَّهُ فَأَصَمَّهُمْ وَأَعْمَىٰ أَبْصَارَهُمْ ﴿24﴾
أَفَلَا يَتَدَبَّرُونَ اَلْقُرْءَانَ أَمْ عَلَىٰ قُلُوبٍ أَقْفَالُهَا ﴿25﴾ إِنَّ اَلَّذِينَ اَرْتَدُّواْ
عَلَىٰ أَدْبَارِهِم مِّنۢ بَعْدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ اُلْهُدَى اَلشَّيْطَٰنُ سَوَّلَ لَهُمْ وَأَمْلَىٰ لَهُمْ ﴿26﴾
ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ قَالُواْ لِلَّذِينَ كَرِهُواْ مَا نَزَّلَ اَللَّهُ سَنُطِيعُكُمْ فِي بَعْضِ اِلْأَمْرِ
وَاللَّهُ يَعْلَمُ أَسْرَارَهُمْ ﴿27﴾ فَكَيْفَ إِذَا تَوَفَّتْهُمُ اُلْمَلَٰٓئِكَةُ يَضْرِبُونَ
وُجُوهَهُمْ وَأَدْبَارَهُمْ ﴿28﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمُ اُتَّبَعُواْ مَا أَسْخَطَ اَللَّهَ
وَكَرِهُواْ رِضْوَانَهُۥ فَأَحْبَطَ أَعْمَالَهُمْ ﴿29﴾

ثمن

18. Wađanda suka shiriya (sune mu-minai) Allah ya Rara masu shi-riyassu ya kimsa musu tsoron Ubangijinsu.
19. To basa sauraron komai (su kaf-iran Makka) saitashin alƙiyama bada tanaji ba, amma alamo-minta sun zo musu (sune aiko ma'aikin Allah sallallahu alaihi wasallama da kecewar watada hayaKi) to yayagargađinsu zai amfanesu in alƙiyama tazo musu.

(LAZIMI NA SUFAYE DASUKE BA WA MURIDAI SHINE HAILALA DA ISTIGFARI)

20. (Ka dauwama) kai sanin cewq ba abin bautawa da gaskiya sai Allah, ka nemi gafara don zunu-binka, don (an fađa masa wan-nan tareda ismassa, saboda al'umarsa su kwaikwaye shi Annabi sallallahu alaihi wasallama ya aikatashi, haƙiƙa ni ina neman gafara sau (fari a kul-lum). Kuma ka nemi gafara ga muminai maza da mata (akwai girmama su da umarnin Anna-binsu da neman gafara garesu muraƙabada mushahada. Allah yasan kaikawonkuda rana, da komawarku izuwa wajen kwan-ciyarkuda daddare (ba abinda yake buyagareshi to ku kiyaye shi).

(MUMINAI NA GASKIYA DA MUNAFUKAI)

21. Wađanda suka fađa (don neman yaƙi) "Me yasa ba a saukar dasura ba, wacce ambaton yald yake cikinta? Idan aka saukar dasura ingatacciya, wacce ba a shafe komai daga gare ta ba aka ambaci neman yaƙi cikinta, sai ka ga wađanda munafinci yake cikin zuciyarsu suna duba izuwa gareka duba irin duban wanda akayi su ma a kansu, (ma'ana duban wanda mutuwa ta zaike masa) don.tsoron mutuwa, saboda haka su suna jin tsoron yaƙi suna Idnsa, to abinda yafi amfa-ni garesu.
22. Da'a da magana kyakkyawa, to idan al'amari ya wajabta, (wato aka wajabta yaƙi), to dasun gasgata Allah a cikin da'a da imani ga Allah dayafi amfani garesu.
23. To watakila kun kusata inkun bijire ga buran imani kuyi bar-na a bayan ƙasa, ku yanyanke zumuncinku, (wato ku koma cikin al'amarin jahiliya na zalinci da kashe-kashe).
24. Wađancananka mabarnatan nan sune wađanda Allah ya tsine musu albarka, yakummtar dasu ga buran gaskiya, ya makan-tar da idandunansu ga buran ga-nin hanyar shiriya.
25. Shin basa lura da alƙur'ani bane? (Sunsan gaskiya) barii rufe-rufen zukata ne a kan zuka-ta, (saboda haka basu fahimce shi ba).
26. Haƙiƙa wađannan da sukayi ridda da munafinci bayan gaskiya ta baiyana garesu, shaiđan ne ya Rawata musu, ya basu shifta, (shi shaiđan ne ya baddasu da nufin Allah).
27. Wancanenka (ɓatarwa) saboda su , sunce ga waifannan dasu-kald abinda Allah ya saukar, "da sannu zamu bi ku a cikin ba'alin lamari, (wato taimako a cikin gabada Annabi sallallahu alaihi wasallama da sanyaya gwiwa ga mutane ta buran yaƙi, wannan maganar sun fadeta ne a asirce, sai Allah ya tsinkayar da manzon Allah sallallahu alai-hi wasallama.) Allah yasan asi-rinsu.
28. Yaya halinsu zai kasance idan Mala'iku suka karɓi ransu suna dukan fuskokinsu da bayaiya-kinsu (da gudumai na baƙin karfe).
29. Wancananka mutuwa kan wan-nan hali saboda cewa su sun bi abinda ya fusata Allah sun ƙi yardar Allah sai Allah ya tar-watsa aikinsu.

أَمْ حَسِبَ الَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٌ أَن لَّن يُخْرِجَ اللَّهُ أَضْغَانَهُمْ (30)
وَلَوْ نَشَاءُ لَأَرَيْنَاكَهُمْ فَلَعَرَفْتَهُم بِسِيمَاهُمْ وَلَتَعْرِفَنَّهُمْ فِي لَحْنِ الْقَوْلِ
وَاللَّهُ يَعْلَمُ أَعْمَالَكُمْ (31) وَلَنَبْلُوَنَّكُمْ حَتَّى نَعْلَمَ الْمُجَاهِدِينَ مِنكُمْ
وَالصَّابِرِينَ وَنَبْلُوَ أَخْبَارَكُمْ (32) إِنَّ الَّذِينَ كَفَرُوا وَصَدُّوا
عَن سَبِيلِ اللَّهِ وَشَاقُّوا الرَّسُولَ مِن بَعْدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ الْهُدَى لَن يَضُرُّوا
اللَّهَ شَيْئًا وَسَيُحْبِطُ أَعْمَالَهُمْ (33) * يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا أَطِيعُوا اللَّهَ وَأَطِيعُوا
الرَّسُولَ وَلَا تُبْطِلُوا أَعْمَالَكُمْ (34) إِنَّ الَّذِينَ كَفَرُوا وَصَدُّوا
عَن سَبِيلِ اللَّهِ ثُمَّ مَاتُوا وَهُمْ كُفَّارٌ فَلَن يَغْفِرَ اللَّهُ لَهُمْ (35)
فَلَا تَهِنُوا وَتَدْعُوا إِلَى السَّلْمِ وَأَنتُمُ الْأَعْلَوْنَ وَاللَّهُ مَعَكُمْ
وَلَن يَتِرَكُمْ أَعْمَالَكُمْ (36) إِنَّمَا الْحَيَاةُ الدُّنْيَا لَعِبٌ وَلَهْوٌ
وَإِن تُؤْمِنُوا وَتَتَّقُوا يُؤْتِكُمْ أُجُورَكُمْ وَلَا يَسْأَلْكُمْ أَمْوَالَكُمْ (37)
إِن يَسْأَلْكُمُوهَا فَيُحْفِكُمْ تَبْخَلُوا وَيُخْرِجْ أَضْغَانَكُمْ (38) هَا أَنتُمْ
هَؤُلَاءِ تُدْعَوْنَ لِتُنفِقُوا فِي سَبِيلِ اللَّهِ فَمِنكُم مَّن يَبْخَلُ وَمَن يَبْخَلْ
فَإِنَّمَا يَبْخَلُ عَن نَّفْسِهِ وَاللَّهُ الْغَنِيُّ وَأَنتُمُ الْفُقَرَاءُ وَإِن تَتَوَلَّوْا
يَسْتَبْدِلْ قَوْمًا غَيْرَكُمْ ثُمَّ لَا يَكُونُوا أَمْثَالَكُم (39)

ربع

30. Bari! Wađanda munafinci yake cikin zuciyarsu sun zaci Allah bazai baiyana Kulle-Kullensu (ga ma'aiki sallallahu alaihi wa-sallama bada muminai).
31. Da mun ga dama da mun nuna maka su, to da sannu zaka sansu, da alamarsu, wallahi zaka sansu a cikin katobarar zance (Shine suyigigazzana da mu-nanan al'amarin musulmi). Allah yasan aikace-aikacenku.
32. Lallai zamu jarrabe ku (dayaƙi da waninsa,) har mu nuna masu ^oKari daga cikinkuda masu dauriya, a cikin yaƙi da wanin-sa, zamu baiyana labaranku, (na daga da'arkuda sabonku a cikin yaƙi da waninsa).
33. Haƙiƙa wađannan da suka kafir-ta, suka hana mutane bin Allah, suka sabawa manzon Allah (sal-lallahu alaihi wasallama), bayan gaskiya ta baiyana garesu, basu cuci Allah komai ba, har abada da sannu zai lalata aiyukansu (sadaka da waninta bazasu ga sakamako ba a lahira. Wannan ta sauka ne a cikin masu baiwa kafirai abinci ranar Badar, ko Kuraizatu da Nadri).

(WAJABCIN DA'AR ALLAH TA'ALA DA MA'AIKINSA)

34. Yaku wađanda kuka bada gaskiya! kubi Allah kubi ma'aikinsa (Sallallahu alaihi wasallama), ka daku ,ɓata ai-kace-aikacenku (da sabonni).
35. Haƙiƙa wađanda suka kafirta suka hana mutane ga buran han-yar Allah (wato shiriya) sannan suka mutu alhali suna kafirai, har abada Allah bazai gafarta musu ba, (ta sauka ne cikin mu-tanen rijiyar Badar).
36. To kada ky yi sauri kada kuyi kira izuwa sulhu tareda kafirai inkun gamu dasu, haƙiƙa kune marinjaya, Allah yana taredaku ,(da taimako da nasara), bazai tauye maku sakamakon ayy-ukanku ba.
37. Haƙiƙa dai rayuwar duniya (wato shagala da ita) wasanni, ne da shagala ga buran Ubangi-ji. In kuka bada gaskiyakukaji tsoron Allah to zai baku sakam-akon ayyukanku, bazai tambay-eku (dukkan) dukiyoyinku ba.
38. In ya tambayeku ita (baki đaya) ya lamtaceku sai kuyi rowa, sai yafitar da bakar gabarku (ga addinin muslunci).
39. To yau kuma ga ku yaku wađannan, ana kiran ku domin ku ciyar a cikin inganta Addinin Allah abinda ya wajabtashi a kanku, to akwai daga cikinku wanda yayi rowa, kuma zai zoda abinda ya rowa dashi din nan, wanda ya, yi rowa to dahir dai yayi rowa ne ga kansa. Allah mawadaci ne ga buran abinda kuke ciyarwa, ko ga buran kabaldnku, kune talakawa fu-tuk izuwa ga Ubangiji. Idan kuka juya bayaga buran da'arsa, zai musanya mutane baku ba yasanya su maimakon ku, sannan bazasu zama kamar ku ba a cikin juya bayaga buran da'a ba, bari! zasu kasance masu da'a gareshi.

48 سُورَةُ الفَتْحِ مَدَنِيَّة
وَهِيَ تِسْعٌ وَعِشْرُونَ ءَايَةً 29

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

إِنَّا فَتَحْنَا لَكَ فَتْحًا مُّبِينًا ﴿1﴾ لِّيَغْفِرَ لَكَ اللَّهُ مَا تَقَدَّمَ مِن ذَنبِكَ وَمَا تَأَخَّرَ
وَيُتِمَّ نِعْمَتَهُ عَلَيْكَ وَيَهْدِيَكَ صِرَاطًا مُّسْتَقِيمًا ﴿2﴾ وَيَنصُرَكَ اللَّهُ نَصْرًا
عَزِيزًا ﴿3﴾ هُوَ الَّذِي أَنزَلَ السَّكِينَةَ فِي قُلُوبِ الْمُؤْمِنِينَ لِيَزْدَادُوا إِيمَانًا
مَّعَ إِيمَانِهِمْ وَلِلَّهِ جُنُودُ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ وَكَانَ اللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمًا ﴿4﴾
لِّيُدْخِلَ الْمُؤْمِنِينَ وَالْمُؤْمِنَاتِ جَنَّاتٍ تَجْرِي مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَارُ خَالِدِينَ فِيهَا
وَيُكَفِّرَ عَنْهُمْ سَيِّئَاتِهِمْ وَكَانَ ذَٰلِكَ عِندَ اللَّهِ فَوْزًا عَظِيمًا ﴿5﴾ وَيُعَذِّبَ الْمُنَافِقِينَ
وَالْمُنَافِقَاتِ وَالْمُشْرِكِينَ وَالْمُشْرِكَاتِ الظَّانِّينَ بِاللَّهِ ظَنَّ السَّوْءِ عَلَيْهِمْ دَائِرَةُ السَّوْءِ
وَغَضِبَ اللَّهُ عَلَيْهِمْ وَلَعَنَهُمْ وَأَعَدَّ لَهُمْ جَهَنَّمَ وَسَاءَتْ مَصِيرًا ﴿6﴾ وَلِلَّهِ جُنُودُ السَّمَاوَاتِ
وَالْأَرْضِ وَكَانَ اللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمًا ﴿7﴾ * إِنَّا أَرْسَلْنَاكَ شَاهِدًا وَمُبَشِّرًا وَنَذِيرًا ﴿8﴾ ثمن
لِّتُؤْمِنُوا بِاللَّهِ وَرَسُولِهِ وَتُعَزِّرُوهُ وَتُوَقِّرُوهُ وَتُسَبِّحُوهُ بُكْرَةً وَأَصِيلًا ﴿9﴾ إِنَّ الَّذِينَ
يُبَايِعُونَكَ إِنَّمَا يُبَايِعُونَ اللَّهَ يَدُ اللَّهِ فَوْقَ أَيْدِيهِمْ فَمَن نَّكَثَ فَإِنَّمَا
يَنكُثُ عَلَىٰ نَفْسِهِ وَمَنْ أَوْفَىٰ بِمَا عَاهَدَ عَلَيْهُ اللَّهَ فَسَيُؤْتِيهِ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿10﴾

WANNAN SURA ITACE SURATUL FATAHI
A MADINA AKA SAUKARDAITA. AYA ISHIRIN DA TARA CE (29)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinkan Muminai a Lahira a keɓe

(SULHUN HUDEBIYA] SABABIN SAUKAR WANNAN SURA AN AMBACE SHI A CIKIN SIYARU WANDA YAKE SON BAYANIN WANNAN SURA YA DUBA LITTAFIN BUHARI DA MUSILIM DA SAURANSU)

1. Haƙiƙa munyi hukunci da bude Makka da waninta mai gaba-towa da zaka buɗe da karfi dayaji, wandazai afku bayan wan-nan sulhu, bude wa mabaiyani.
2. Domin Ubangiji ya gafarta maka abinda yagabata (saboda yaƙinka) na daga zunubinka da abinda yajinkirta (donka kwadaitar da al'ummarka a cikin yaƙi wato ana nufin zunu-ban al'umma tasa saboda anna-bawa abadan kiyayewa ne daga zunubi, ta fuskar dalilin hankali yankakke) ya cika ni'imarsa a | gareka (da wannan fatahin) ya shiryeka (da wannan fatahin ta-farki madaidaici Shine musu-lunci.
3. Allah ya taimakeka (dashi) tai-mako mabuwayi (wato wanda babu wulaKanci tare dashi har abada).
4. Shine wanda ya saukar da nutsu-wa cikin zukatan muminai donsu kara imani tareda imaninsu (da shari'o'in addini dukkansu, kodayaushe (faya ta sauka daga gareta, saisu bada gaskiya da ita, yaƙi yana daga cikinta,) mn-dunar sammai da ƙassaina Allah ne (da Allah yanufi taima-kon addininsa badaku ,ba, da saiya aikata), Ubangiji masanine (da halittarsa) gwanine (cikin aikinsa, bai gushe ba mai si-fantuwa da wancanenka.)

(WANDA SUKA KUDURA ALKAWARI DA ALLAH TAREDA MANZONSA S.A.W.)

5(Yayi umarni dayald ne) domin ya shigad da muminai maza da mata aljannatai da ƙoramu sukc gudana karƙashinta masu dau-wama a cikinta ya kankare musu miyagun ayyukansu wan-canenka ya kasance mai girma gurin Ubangiji.

6. Yayiwa munafikai maza da mata azaba masuyin zato da Allah (sun zaci cewa shi Ubangiji bazai taimaki annabi sallallahu alaihi wasallama ba,) girmama ta azabada wulaƙanci maga-miya ta tabbata a kansu. Allah yayi fushi a kansu ya tsine musu, kuma ya tanaji Jahanna-ma domin su.
7. Rundunar sammai da ƙassaina Allah ne Ubangiji ya tabbata mabuwayi (cikin mulkinsa), gwani (cikin aikinsa).

(BARARRAJEWAR SHUGABASALLALLAHU ALAIHI WA SALLAMA AKAN KARAGAR HILAFAR UBANGIJI WACCE TA ZAMA SAMA DA HILAFAR ANNADI ADAMU ALAIHISSALAMU)

8. Haƙiƙa mun aiko ka mai shedar-wa (bisa al'ummarka da da'a da sabo a ranar alƙiyama,) mai albishir (da aljanna,) mai gargaɗi (da wuta a cikinta ga wanda ya aikata mummunan aiki).
9. Don ku bada gaskiya da- Allah da ma'aikinsa, ku taimake shi ku girmama shi, kuyi tasbihi ga Allah safiya dayammaci.
10. Haƙiƙa waɗannan dasuke yin caffa da kai, (caffar yarda a Hu-debiya,) ga Allah suke yin caffa kawai, rahamar Allah ce burbu-shin hannayensu (wacce sukayi mubaya'a da ita; ai Ubangiji mai tsinkaye ne a kan caffar da suka yi, zai musu sakamako a kanta). Wanda ya warware ta ya warware ne ga kansa (saboda shi zai ɗanɗani kudarsa,) wanda ya cika da abinda yayi wa Allah alkawari a kansa, (Ubangiji yace) "da sannu zamu bashi lada maigirma".

(Masu jinkiri ga buran Hudebiya)

سَيَقُولُ لَكَ ٱلْمُخَلَّفُونَ مِنَ ٱلْأَعْرَابِ شَغَلَتْنَآ أَمْوَٰلُنَا وَأَهْلُونَا فَٱسْتَغْفِرْ لَنَا
يَقُولُونَ بِأَلْسِنَتِهِم مَّا لَيْسَ فِى قُلُوبِهِمْ قُلْ فَمَن يَمْلِكُ لَكُم مِّنَ ٱللَّهِ شَيْـًٔا إِنْ أَرَادَ بِكُمْ
ضَرًّا أَوْ أَرَادَ بِكُمْ نَفْعًۢا بَلْ كَانَ ٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرًا ﴿11﴾ بَلْ ظَنَنتُمْ أَن لَّن
يَنقَلِبَ ٱلرَّسُولُ وَٱلْمُؤْمِنُونَ إِلَىٰٓ أَهْلِيهِمْ أَبَدًا وَزُيِّنَ ذَٰلِكَ فِى قُلُوبِكُمْ وَظَنَنتُمْ ظَنَّ
ٱلسَّوْءِ وَكُنتُمْ قَوْمًۢا بُورًا ﴿12﴾ وَمَن لَّمْ يُؤْمِنۢ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ فَإِنَّآ أَعْتَدْنَا
لِلْكَـٰفِرِينَ سَعِيرًا ﴿13﴾ وَلِلَّهِ مُلْكُ ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ يَغْفِرُ لِمَن يَشَآءُ
وَيُعَذِّبُ مَن يَشَآءُ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿14﴾ سَيَقُولُ ٱلْمُخَلَّفُونَ
إِذَا ٱنطَلَقْتُمْ إِلَىٰ مَغَانِمَ لِتَأْخُذُوهَا ذَرُونَا نَتَّبِعْكُمْ يُرِيدُونَ أَن يُبَدِّلُوا۟ كَلَـٰمَ ٱللَّهِ
قُل لَّن تَتَّبِعُونَا كَذَٰلِكُمْ قَالَ ٱللَّهُ مِن قَبْلُ فَسَيَقُولُونَ بَلْ
تَحْسُدُونَنَا بَلْ كَانُوا۟ لَا يَفْقَهُونَ إِلَّا قَلِيلًا ﴿15﴾ قُل
لِّلْمُخَلَّفِينَ مِنَ ٱلْأَعْرَابِ سَتُدْعَوْنَ إِلَىٰ قَوْمٍ أُو۟لِى بَأْسٍ شَدِيدٍ
تُقَـٰتِلُونَهُمْ أَوْ يُسْلِمُونَ فَإِن تُطِيعُوا۟ يُؤْتِكُمُ ٱللَّهُ أَجْرًا حَسَنًا
وَإِن تَتَوَلَّوْا۟ كَمَا تَوَلَّيْتُم مِّن قَبْلُ يُعَذِّبْكُمْ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿16﴾ لَّيْسَ عَلَى ٱلْأَعْمَىٰ
حَرَجٌ وَلَا عَلَى ٱلْأَعْرَجِ حَرَجٌ وَلَا عَلَى ٱلْمَرِيضِ حَرَجٌ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ
نُدْخِلْهُ جَنَّـٰتٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَـٰرُ وَمَن يَتَوَلَّ نُعَذِّبْهُ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿17﴾

11. Da sannu masu jinkiri ga buran fitar yaƙin Hudebiya na daga Larabawan kauye (waɗanda suke daura da Madina, waɗanda Allah yajinkirtar dasu ga buran abutarka yayin daka nemi fita dasu izuwa Makka, don tsoron tasowar ƙuraishawa gareka, a shekarar Hudebiya m ka koma gareta,) zasu ce da kai, "du-kiyoyinmune suka shagalar da mu da iyalinmu ga buran fita tareda kai, ka nemi Allah yayi mana gafara", (Ubangiji yace dasu, yana mai ƙaryatawa garesu,) "suna faɗa da harasansu na daga neman gafara da harasan-su, na daga abinda ba a cikin zukatansu yake ba, su masu ƙarya ne a hanzarinsu, to ce ne dasu, "to wanene zai mallaki wani abu naku daga Allah in yanufi cutarku ko yanufi anafani da ku?". Bari! Allah masanine da abinda kuke aikatawa.

12. Bari! Ku dai kun zaci manzon Allah (Sallallahu alaihi wa Sal-lama) da muminai bazasu koma izuwa iyalinsu ba har aba-da. An Kawata wancanenka zu-katanku, (cewa za a tumbuke su bazasu koma gida ba,) kun yi zato mummunan zato kun ka-sance mutane halakakku, (saboda wannan zato nan ga Allah).

13. Wanda bai bada gaskiya da Allah da ma'aikinsa ba, to haƙiƙa mu mun tanadi wuta mai tsana-nin azaba ga kafirai.

14. Mulkin sammai da ƙassaiya tabbata ga Allah, yana gafara ga wanda yaga dama, yana azaba ga wanda yaga dama, Ubangiji ya tabbata mai gafara mai raha-ma.

15. Da sannu masu jinkirin nan zasu faɗa idan kun tafi izuwa ga-nimomin da aka samu daga Hai-bara don ku karbeta "ku bar mu mu bi ku (don mu samu daga gareta)" suna nufin su musanya zancen Ubangiji. Ce ne dasu, "bazakubi mu ba har abada, haka Allah yace tun gaban (ko-mowarmu)". Da sannu zasu ce:
"Bari! kunayi mana hassada ne". Bari! sun kasance basa hankaltar (addini sai kaɗan daga garesu).

16. Ka faɗa ga masu jinkirin nan "da sannu za a kira ku izuwa mutane ma'abuta yaƙi mai tsa-nani (Ance sune Banu Hanifa mutanen Yamana h, Kuma Ance Farisa da Rum) da zakuyi yake-yake dasu, ko su musul-lunta (bazakuyi yake-yake dasu ba,) idan kukabi izuwa yaƙi dasu Allah zai baku lada mai yawa, idan kuka juya baya ka-mar yadda kuka juya a da can, Allah zaiyi maku azaba, azaba mai raɗaɗi.

17. Ba laifi bisa makaho, (a cikin barin yaƙi) haka nan ba laifi kan gurgu, ba laifi ga maralafiya, wanda yabi Allah, zamu shig-ad dashi aljanna, wanda ya juya da baya zamuyi masa azaba mai raɗaɗi.

حزب

* لَقَدْ رَضِيَ اللَّهُ عَنِ الْمُؤْمِنِينَ إِذْ يُبَايِعُونَكَ تَحْتَ الشَّجَرَةِ فَعَلِمَ مَا فِي قُلُوبِهِمْ
فَأَنزَلَ السَّكِينَةَ عَلَيْهِمْ وَأَثَابَهُمْ فَتْحًا قَرِيبًا ﴿18﴾ وَمَغَانِمَ كَثِيرَةً يَأْخُذُونَهَا
وَكَانَ اللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمًا ﴿19﴾ وَعَدَكُمُ اللَّهُ مَغَانِمَ كَثِيرَةً تَأْخُذُونَهَا
فَعَجَّلَ لَكُمْ هَٰذِهِ وَكَفَّ أَيْدِيَ النَّاسِ عَنكُمْ وَلِتَكُونَ ءَايَةً لِّلْمُؤْمِنِينَ
وَيَهْدِيَكُمْ صِرَاطًا مُّسْتَقِيمًا ﴿20﴾ وَأُخْرَىٰ لَمْ تَقْدِرُوا عَلَيْهَا قَدْ
أَحَاطَ اللَّهُ بِهَا وَكَانَ اللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرًا ﴿21﴾
وَلَوْ قَاتَلَكُمُ الَّذِينَ كَفَرُوا لَوَلَّوُا الْأَدْبَارَ ثُمَّ لَا يَجِدُونَ وَلِيًّا
وَلَا نَصِيرًا ﴿22﴾ سُنَّةَ اللَّهِ الَّتِي قَدْ خَلَتْ مِن قَبْلُ
وَلَن تَجِدَ لِسُنَّةِ اللَّهِ تَبْدِيلًا ﴿23﴾ وَهُوَ الَّذِي كَفَّ أَيْدِيَهُمْ
عَنكُمْ وَأَيْدِيَكُمْ عَنْهُم بِبَطْنِ مَكَّةَ مِنۢ بَعْدِ أَنْ أَظْفَرَكُمْ عَلَيْهِمْ
وَكَانَ اللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرًا ﴿24﴾ هُمُ الَّذِينَ كَفَرُوا
وَصَدُّوكُمْ عَنِ الْمَسْجِدِ الْحَرَامِ وَالْهَدْيَ مَعْكُوفًا أَن يَبْلُغَ مَحِلَّهُ
وَلَوْلَا رِجَالٌ مُّؤْمِنُونَ وَنِسَاءٌ مُّؤْمِنَاتٌ لَّمْ تَعْلَمُوهُمْ أَن تَطَئُوهُمْ
فَتُصِيبَكُم مِّنْهُم مَّعَرَّةٌ بِغَيْرِ عِلْمٍ لِّيُدْخِلَ اللَّهُ فِي رَحْمَتِهِ مَن يَشَاءُ
لَوْ تَزَيَّلُوا لَعَذَّبْنَا الَّذِينَ كَفَرُوا مِنْهُمْ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿25﴾

(BAI'ATU RILWANI DA ABINDA YAKE CIKINTA NA ALHERI)

18. Haƙiƙa Ubangiji ya yarda ga muminai zamanin da sukayi mubaya'a da kai, a Hudebiya (wato sukayi caffa) Karkashin itaciya, (wato Itace itaciyar ay-aba. Ko da yake ana ce da ita farar Kaya) su dubu ne da dari uku, ko son fi haka, sannan yayi mubaya'a dasu a bisa su far-ma kuraishu kuma bazasu guje wa mutuwa ba,) sai Allah yasan abinda yake zukatansu (na daga gaskiya da cikawa, saiya saukar da nutsuwa a garesu,) ya saka musu budi makusanci, (Shine fatahu Haibara, bayan ko-mowarsu daga Hudebiya).

19. (Yakuma alƙawarta masu) ribo-bi masu yawa, dasuke karbarta daga Haibara, Ubangiji ya tab-bata mabuwayi mai hikima.

20. Allah yayi muku alkawarin ga-nimomi masu yawa, da zaku same ta (daga bude-bude,) sai yagaggauta muku ganimar Hai-bara, ya kame hannuwan mu-tane ga buran ku a cikin iyalin-ku, (yayin da kuka fita, Yahudawa sukayi nufin su far musu, sai Ubangiji ya jefa raza-ni cikin zukatansu, kuma don (ita wannan ganima abar gag-gautawa) ta kasance ayaga mu-minai, (su gode masa a kanta). Ya shirye ku tafarki madaidaici.

21. Wadansu ganimomin kuwa baku sami iko a kanta ba (Itace Farisa da Rum) haƙiƙa Allah ya kewaye da saninta, (yasan cewa itada sannu zata kasance gare-ku,) Ubangiji ya tabbata mai iko bisa komai.

22. Da Waɗanda suka kafurta sun yaƙe ku (a Hudebiya) dasun bada baya (sun girka a guje), san-nan bazasu sami wani mai kiyayewa dazai kiyaye su ba, wala mai taimako.

23. (Risbakafirai da taimakon mu-minai ya zama) sunnar Allah wacce ta wuce tun can gaba, bazaka sami musanyaga sunnar Allah ba.

24. Shine wanda ya kiyaye Hannu-wansu ga buran kuda hannu-wanku ga buran su a cikin Mak-ka (a Hudebiya), bayan ya rinjayar daku ,a kansu (saboda 80 daga garesu sun kewaye san-saninku donsu samu daga gareku aka kamo su aka kawo su ga ma'aikin Allah sallallahu alihi wasallama yayi musu rang-wame ya sake su, sai wannan ya zama sababin sulhu), Ubangiji yasan abinda kuke aikatawa zaiyi muku sakamako.

25. Sune waɗanda suka kafirta, suka hana ku saduwa da masal-laci mai alfarma suka hana ha-dayarku a daure, suka hana ta isa gurin wanda ake soke ta a al'ada, (Shine Harami), ba don mazaje muminai ba, da mataye muminai (waɗanda suke tareda kafirai a Makka) da baku san su ba, ku tatsile su (tareda kafi-rai da an yi izini gareku a cikin bude Makka), sai laifi ya same ku daga garesu, bada saninku dasu ba, domin Ubangiji ya shigad da wanda yaga dama cikin jinkansa, (kamar waɗannan muminai abadan ambato), da muminai sun ware guri (faya, ga buran kafirai, da mun azabci waɗanda suka kafirta daga gare-su (mutanen Makka) azaba mai raɗaɗi.

إِذْ جَعَلَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ فِى قُلُوبِهِمُ ٱلْحَمِيَّةَ حَمِيَّةَ
ٱلْجَٰهِلِيَّةِ فَأَنزَلَ ٱللَّهُ سَكِينَتَهُۥ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَعَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ
وَأَلْزَمَهُمْ كَلِمَةَ ٱلتَّقْوَىٰ وَكَانُوٓا۟ أَحَقَّ بِهَا وَأَهْلَهَا
وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمًا ﴿26﴾ ۞ لَّقَدْ صَدَقَ
ٱللَّهُ رَسُولَهُ ٱلرُّءْيَا بِٱلْحَقِّ لَتَدْخُلُنَّ ٱلْمَسْجِدَ ٱلْحَرَامَ
إِن شَآءَ ٱللَّهُ ءَامِنِينَ مُحَلِّقِينَ رُءُوسَكُمْ وَمُقَصِّرِينَ
لَا تَخَافُونَ فَعَلِمَ مَا لَمْ تَعْلَمُوا۟ فَجَعَلَ مِن دُونِ ذَٰلِكَ فَتْحًا
قَرِيبًا ﴿27﴾ هُوَ ٱلَّذِىٓ أَرْسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلْهُدَىٰ وَدِينِ ٱلْحَقِّ
لِيُظْهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّينِ كُلِّهِۦ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدًا ﴿28﴾
مُّحَمَّدٌ رَّسُولُ ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلْكُفَّارِ رُحَمَآءُ بَيْنَهُمْ
تَرَىٰهُمْ رُكَّعًا سُجَّدًا يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضْوَٰنًا
سِيمَاهُمْ فِى وُجُوهِهِم مِّنْ أَثَرِ ٱلسُّجُودِ ذَٰلِكَ مَثَلُهُمْ فِى ٱلتَّوْرَىٰةِ
وَمَثَلُهُمْ فِى ٱلْإِنجِيلِ كَزَرْعٍ أَخْرَجَ شَطْـَٔهُۥ فَـَٔازَرَهُۥ فَٱسْتَغْلَظَ فَٱسْتَوَىٰ
عَلَىٰ سُوقِهِۦ يُعْجِبُ ٱلزُّرَّاعَ لِيَغِيظَ بِهِمُ ٱلْكُفَّارَ وَعَدَ ٱللَّهُ
ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِنْهُم مَّغْفِرَةً وَأَجْرًا عَظِيمًا ﴿29﴾

ثمن

26. Zamanin da wađanda suka kafir-ta suka sanya marin baya (wato toma da takabburanci) irin to-mar Jahiliyya (Itace hana Anna-bi Sallallahu alaihi wa sallama da Sahabbansa masallaci mai al-farma) sai Ubangiji ya saukar da nutsuwarsa ga manzonsa da kuma muminai (sai sukayi sul-hu dasu a kan su komo daga shekara mai zuwa, abinda ya sami kafirai na takabburanci bai sami su muminai ba, saboda haka basu yalce su ba,) ya la-zumta wa muminai kalmar tsoron Allah, (wato LA ILAHA IL-LALLAHU, MUHAMMADUR RASULULLAHI SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAMA, an lika ta izuwa takawa domin Itace sababinta,) sun kasance sune mafiya cancantada ita (wannan kalmar daga kafirai) sun ka-sance mazowan kalmar takawa, haƙiƙa Ubangiji ya tabbata ma-sanine da kowane abu.

(TABBATAR DA MAFARKIN SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAMA)

27. Haƙiƙa Ubangiji yagasgatawa manzonsa mafarkinsa da gaskiya, (Manzon Allah yayi ma-farki a zamanin, cewa shi haƙiƙa yana shiga Makka shi da Sahabbansa, suna cikin aminci,' suna aski suna saisaye, ya basahabbansa labari da wancanan-ka sukayi muma, a zamanin da suka fito tare dashi, kafirai suka hana shi shiga dakin KA'ABA a Hudebiya suka koma gida, wannan yayi ta kawo damuwa garesu, ba'alin munafikai kuma suka shiga cikin kokonto, sai Allah ya saukad da ita wannan aya,) Wallahi zaku shigo cikin masallaci mai alfarma in Allah ya yarda kuna amintattu masu aske kawukan-kuda masu saisaye ba"alin ga-sunsu, bazakuji tsoro ba har abada, to Allah yasan abinda baku sani ba cikin sulhun nan na daga gyattuwa, sai yasanya budi daga budl makusanci (Shine bude Haibara, mafarkin kuma yagasgata.)

(ALBISHIR DA TABBATAR SUFANCI HAR ABADA)

28. Shine wanda ya aiko manzonsa dashiriya da addinin gaskiya domin ya rinjayad dashi a kan addinai dukkansu. Ubangiji ya isa shaida (a kan cewa kai man-zo ne da abinda aka anbata.)

(KIRARI GA ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAMA DA SAHABBANSA ALLAH YA KARA MUSU YARDA)

29. Annabi Muhammadu (Sallallahu alaihi wa sallama) manzon Allah ne, wađanda suke tare dashi (na Sahabbansa), ƙarfafe ne a kan kafirai (basa tausayinsu) masu jinƙai ne a tsakanin junan-su, (suna tausayawa juna suna ƙaunar juna kamar ubada dansa), kana ganinsu suna masu sunkuyo masu dungura goshi, suna neman falala daga Ubangi-ji dayarda, alamarsu tana cikin fuskokinsu saboda gaisuwa ga Ubangiji, wancanenka sifa abin anbato Shine sifarsu cikin At-taura. Misalinsu kuwa a cikin Linjila kamar hatsi ne dayafi-tar da tsakinsa, ya taimake shi, sai yayi kauri, yayi daidai a kan makyangyamarsa, yana bai-wa manoma sha'awa (saboda kyansa, Allah ya tcara yarda a garesu amin. Allah ya sifantasu da wannan, saboda su sun fara ne cikin karanci da rauni suka yawaita suka karfafa kan mafi kyan fuskoki,) donya fusata ka-firai, Allah ya alkawarta wa wa-danda suka bada gaskiya sukayi aiki nagari daga cikinsu gafa-ra da lada mai girma. (Ga farar da lada mai girma ya tabbata ga wađanda zasu zo bayansu. Sa-boda anfanin wannan aya masa-na Allah suka rilee ta binni mai katangancewa).

49 سُورَةُ الحُجُرَاتِ مَدَنِيَّة
وهي ثماني عشرة ءاية 18

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

ربع
* يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تُقَدِّمُواْ بَيْنَ يَدَيِ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ
إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٞ ١ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَرۡفَعُوٓاْ أَصۡوَٰتَكُمۡ
فَوۡقَ صَوۡتِ ٱلنَّبِيٓءِ وَلَا تَجۡهَرُواْ لَهُۥ بِٱلۡقَوۡلِ كَجَهۡرِ بَعۡضِكُمۡ لِبَعۡضٍ أَن تَحۡبَطَ
أَعۡمَٰلُكُمۡ وَأَنتُمۡ لَا تَشۡعُرُونَ ٢ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَغُضُّونَ أَصۡوَٰتَهُمۡ عِندَ رَسُولِ ٱللَّهِ
أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ٱمۡتَحَنَ ٱللَّهُ قُلُوبَهُمۡ لِلتَّقۡوَىٰۚ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَأَجۡرٌ عَظِيمٌ ٣
إِنَّ ٱلَّذِينَ يُنَادُونَكَ مِن وَرَآءِ ٱلۡحُجُرَٰتِ أَكۡثَرُهُمۡ لَا يَعۡقِلُونَ ٤
وَلَوۡ أَنَّهُمۡ صَبَرُواْ حَتَّىٰ تَخۡرُجَ إِلَيۡهِمۡ لَكَانَ خَيۡرٗا لَّهُمۡۚ وَٱللَّهُ
غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٥ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن جَآءَكُمۡ فَاسِقُۢ بِنَبَإٖ
فَتَبَيَّنُوٓاْ أَن تُصِيبُواْ قَوۡمَۢا بِجَهَٰلَةٖ فَتُصۡبِحُواْ عَلَىٰ مَا فَعَلۡتُمۡ نَٰدِمِينَ ٦
وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ فِيكُمۡ رَسُولَ ٱللَّهِۚ لَوۡ يُطِيعُكُمۡ فِي كَثِيرٖ مِّنَ ٱلۡأَمۡرِ لَعَنِتُّمۡ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ
حَبَّبَ إِلَيۡكُمُ ٱلۡإِيمَٰنَ وَزَيَّنَهُۥ فِي قُلُوبِكُمۡ وَكَرَّهَ إِلَيۡكُمُ ٱلۡكُفۡرَ وَٱلۡفُسُوقَ
وَٱلۡعِصۡيَانَۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلرَّٰشِدُونَ ٧ فَضۡلٗا مِّنَ ٱللَّهِ وَنِعۡمَةٗۚ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٨

Wannan sura Itace Suratul Hujurati

A Madina aka saukar da ita. Aya goma sha takwas ce (18)

INA FARAWA DASUNAN UBANGUI MAI JINKAN TALDCAI A DUNIYAGABADAYA, MAI JINKAN MUMINAI A LAHIRA A KEBE

(Wannan sura ta tara Makarimul Akhlaki tashiryar da musulmai izuwa gareta ta baiyana musu ladabi tareda shugabasallalla-hu Alaihi wa Sallam a cikin ko wanne hali tareda kuma dayad-da zasu kabaƙi fasikai da abinda zasuyimu'amila da'yan uwansu muminai, suna nan a gabansu ko basa nan. Ta baiyana haƙiƙar imani da muminai da fifikon aiyuka da tadodi manya da wanin wannan).

(LADABTAR DA SAHABBAI DA SAURAN MUMINAI GA SHUGABASALLALLAHM ALAIHI WA SALLAM KODA SMYI WANI ABU BADA [ZININ ALLAH DA MA'AIKINSA BA)

1. Yaku wacTanda suka bada gaskiya da Allah, kada kuyi karanbani da magana koda aiki, ga-ban Ubangiji da ma'aikinsa, mai iyarwa daga Allah, bada iz-ininsu bakuji tsoron Allah, Ubangiji mai ji ne mai gani (da aikinkuda zancenku. Wannan aya ta sauka ne cikin wata jayayya da Abubakar da Umam Allah ya ƙara musu yarda a ga-ban ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wasallama, Manzon Allah yacc «a sarauta Ka'aka'u dan Ma'abudu» Umaru yacc «a sa-rauta Akar'u dan Hadisu». Abu-bakar yace «baka nufi komai basaika saba mini», Umaru yace «ban nufi saba maka ba», sukayi husuma har muryoyinsu ta daga, sai waɗannan ayoyi biyar suka sauka har izuwa faɗinsa gafurun Rahimun).

(LADABIN ZANCE DA MA'AIKIN ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAMA)

(Wannan aya ta sauƙa a cikin wanda ya daukaka muryarsa nan ga Annabi Sallallahu alaihi wa sal-lama).

2. Ya'ku waɗanda kuka bada gaskiya da Allah! kadaku ,daukaka muryoyinky in zakuyi magana burbushin muryar Annabi (Sal-lallahu alaihi wasallama in yana magana) kadaku, baiyana masa da zance (inkuna ganawa dashi), kamar baiyanawar ba'alinky ga ba'ali, (saidai koma-bayan wannan don girma-mawa a gareshi) don kada ayy-ukansu su watsc alhali ku baku sani ba, (baku san wancanenka daukakawa da bayyanawa da aka ambata ba).

(WANNAN AYA TA SAUKA A CIKIN WANDA YAKE RASRASTA MURYARSA DA ABUBAKAR DA UMARU DA WANINSU ALLAH YA ƘARA YARDA A GARESU)

3. Haƙiƙa waɗannan dasukc ƙasƙasta muryarsu ga ma'aikin Allah, haƙiƙa wadancanenka sune waɗanda Ubangiji ya jarrabi zukatansu don tsoron Allah (donta baiyana daga garesu) gafara ta tabbata garesu da lada mai girma (Shine Aljanna).

(WANNAN TA SAUKA NE GA WASUMUTANE DA SUKAZO GARJIN RANA MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAMA YANA CIKIN GIDA SAI SUKA KIRA SHI)

4. Haƙiƙa waɗannan dasuke kiran-ka daga bayan ɗakunan (matay-enka) yawaicinsu basu da han-kali a cikin abinda suke aikatashi, darajarka macTaukakiyace daga abinda yake tare dashi na ta'azimi).

5. Da dai cewa sun haKura har ka fito izuwa garesu daya kasance mafi amfani garesu. Ubangiji mai gafara ne mai jinƙai (ga wanda ya tubadaga cikinsu).(Tafiya a sannu a cikin karbar labarai. Wannan aya ta sauka a cikin Walidu dan Ukba alhali Manzon Allah Sallallahu alaiki wa sallama ya aike shi izuwa bani Musdaliki donya Rarbo Zakka sai yaji tsoro saboda wata sakayya da takc tsakaninsu a zamanin Jahiliyya sai yakomo bai jc basai yace sun hana shi Zakkar sun nufin kashe shi, Manzon Allah 'Sallallahu alaihi wa sallama zai ya£e su, sai sukazo suna musun abinda aka faɗa masa).

6. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya idafi fasiƙi yazo mukuda labari to sai ku tafi a sannu, kada kuyi garajcn ƙaryatashi don kadaku ,samu mutanc da jahilci ku zamo kuna masu nada-ma a kan abinda kuka aikata, (sai Manzon Allah Sallallahu alihi wa sallama ya aiki Khalidu izuwa garesu bayan sun koma izuwa garinsu bai ga komai ba cikinsu sai alheri da

ثمن

* وَإِن طَآئِفَتَانِ مِنَ الْمُؤْمِنِينَ اَقْتَتَلُواْ فَأَصْلِحُواْ بَيْنَهُمَا فَإِنۢ بَغَتِ اِحْدَاهُمَا
عَلَى الْاُخْرَىٰ فَقَاتِلُواْ الَّتِے تَبْغِے حَتَّىٰ تَفِيٓءَ إِلَىٰٓ أَمْرِ اللَّهِ فَإِن فَآءَتْ فَأَصْلِحُواْ
بَيْنَهُمَا بِالْعَدْلِ وَأَقْسِطُوٓاْ إِنَّ اللَّهَ يُحِبُّ الْمُقْسِطِينَ ﴿9﴾
إِنَّمَا الْمُؤْمِنُونَ إِخْوَةٌ فَأَصْلِحُواْ بَيْنَ أَخَوَيْكُمْ وَاتَّقُواْ اللَّهَ
لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ ﴿10﴾ يَٰٓأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا يَسْخَرْ قَوْمٌ مِّن قَوْمٍ عَسَىٰٓ
أَن يَكُونُواْ خَيْراً مِّنْهُمْ وَلَا نِسَآءٌ مِّن نِّسَآءٍ عَسَىٰٓ أَن يَكُنَّ خَيْراً مِّنْهُنَّ
وَلَا تَلْمِزُواْ أَنفُسَكُمْ وَلَا تَنَابَزُواْ بِالْأَلْقَابِ بِئْسَ الِاسْمُ الْفُسُوقُ
بَعْدَ الْإِيمَانِ وَمَن لَّمْ يَتُبْ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ الظَّالِمُونَ ﴿11﴾
يَٰٓأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُواْ اُجْتَنِبُواْ كَثِيراً مِّنَ الظَّنِّ إِنَّ بَعْضَ الظَّنِّ إِثْمٌ
وَلَا تَجَسَّسُواْ وَلَا يَغْتَب بَّعْضُكُم بَعْضاً أَيُحِبُّ أَحَدُكُمُۥٓ أَن يَأْكُلَ لَحْمَ أَخِيهِ مَيِّتاً
فَكَرِهْتُمُوهُ وَاتَّقُواْ اللَّهَ إِنَّ اللَّهَ تَوَّابٌ رَّحِيمٌ ﴿12﴾ يَٰٓأَيُّهَا النَّاسُ إِنَّا خَلَقْنَٰكُم
مِّن ذَكَرٍ وَأُنثَىٰ وَجَعَلْنَٰكُمْ شُعُوباً وَقَبَآئِلَ لِتَعَارَفُوٓاْ إِنَّ أَكْرَمَكُمْ عِندَ اللَّهِ أَتْقَىٰكُمْ
إِنَّ اللَّهَ عَلِيمٌ خَبِيرٌ ﴿13﴾ * قَالَتِ الْأَعْرَابُ ءَامَنَّا قُل لَّمْ تُؤْمِنُواْ وَلَٰكِن قُولُوٓاْ
أَسْلَمْنَا وَلَمَّا يَدْخُلِ الْإِيمَانُ فِے قُلُوبِكُمْ وَإِن تُطِيعُواْ اللَّهَ
وَرَسُولَهُۥ لَا يَلِتْكُم مِّنْ أَعْمَالِكُمْ شَيْئاً إِنَّ اللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿14﴾

ربع

biyayya, saiya baiwa Annabi Sallallahu alaihi wa sallama labari da wan-nan).

7. Ku sani akwai ma'aikin Allah (Sallallahu alaihi wa sallallama) a cikinku (kada kuyi maganar banza), dayana daka taku cikin abinda kuke bashi labari dashi a bisa (sabanin yadda yake), da kun wahala, amma Allah yasoyar da imani izuwa gareku ne, yasanya ƙin yarda da kafirci da fasiƙanci da saɓo izuwa gareku, wadancanenka sune shiryayyu (masu tabbata kan addininsu).
8. Don falala daga Ubangiji da ni'ima (gareku yasanya kin yar-da da kafirci da fajirci daga ga-reku) Ubangiji masani me (da ku) gwanine (cikin ni'imar dayayi muku).

[YADDAZA AYI MAGANIN FITINA 'YA GIDA]

(Wannan aya ta sauka a cikin wata matsala wato Manzon Allah Sallallahu alaihi wa sallama ne ya hau jaki sai jaki yayi bawali, sai dan Ubaiyu ya toshe hancin-sa, sai dan Rawahata yace, Wallahi fitsarin jakinsa yafi al-miskinka ƙanshi, sai doke-doke ya ɓam tsakanin hannayensu guda biyu da takalma da tankar dabino).

9. Idan jama'a guda biyu na muminai sukayi yaƙi wato sukayi basasa to kuyi sulhu a tsakanin-su da nasiha da kira izuwa hu-kuncin Allah, idan dayansu yayi cin zali a kan dava to ku yaƙi wacce tayi cin zali, har ta koma izuwa al'amarn Allah (wato gaskiya), idan ta komo izuwa gaskiya to kuyi gyara a tsaka-ninsu (da adalci, kuyi adalci) halaKa Ubangiji yana son Adi-lai.
10. Tabban su muminai 'yan uwa ne a cikin addini, ku gyara tsakanin 'yan uwanku (in sun yi husu-ma), kuji tsoron Allah (saboda ƙaunar Ubangiji) yayi muku ra-hama.

(WASIYOYI NA UBANGIJI A CIKIN KYAN ZAMA DA ZAMAN TARE)

11. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya,! (ta sauka ne a cikinkungiyar Tamimu yayin da sukayi izgili daga Fuƙara'ul musli-mina kamar Ammaru dasuhai-bu), kada wadansu mutane daga cikinku suyiizgili da wasu yana yiwuwa su kasance mafifi-ta (wajen Allah), wala mata daga cikinku kadasuyiizgili da wasu, yana kusantuwa daga garesu su zama mafifita a wurin Ubangiji. Kadaku ,laifinta kaw-ukanku (wato kada sashenku ya aibata sashe) kada kuyi jefefe-niya da laƙabai, wato kada kuyi zage-zage dasunan kafiri ko fasiRi. Tur! dasuna abin anbato na izgili da laifantawa da zage-zage tur! da fasiƙanci bayan imani wanda bai tuba ba to waɗannan sune ainahin azzalu-mai.
12. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya! ku nisanci yawaicin zato, haƙiƙa shashin zato laifi ne, (ka-mar mummunan zato ga muta-nen Allah, amma mummunan zato ga fasiƙai wannan ba laifi a cikinsa ballantana a cikin abinda suka baiyana kamar shan giya a fili ko caca ko shan taɓa). Kadaku ,binciki (al'aurar mu-sulmi da laifikansu), kada shah-sinku yayi gibar shashi kada ya ambace shi da abinda ba yaso.Yanzu dayanku yana so yaci naman dan uwansa mataccc? A'a, sai kuka ki ci, (to gibassa a cikin rayuwarsa kamar cin na-mansa ne a cikin mutuwarsa,) To kuji tsoron ukubar Ubangiji, haƙiƙa Ubangiji Shine mai karBar tuban masu tuba, mai jinƙai (garesu).

(ILIMIN NASABA)

13. Yaku waɗannan mutanel haƙiƙa mun halicce ku 4aga namiji da mace (Adamu da Hauwa'u) iTiun sanya ku tozayen nasaba ga kabiloli na nasaba (wato ƙasa da tozoda soraye na nasabasannan cikkunan nasabasannan cinyoyin nasabasannan yayyu na nasaba misalinsa a nasabar Annabi Khuzainiatu Sha'aibu ne, Kinanatu kabila ce ta nasa-ba, kuraishi daki ne na nasabakusaiyu ciki ne na nasaba. Ha-shimu cinyace na nasaba, Ab-basu dan yaye ne na nasaba) don ku san juna (badan kuyi alfahari da daukaka nasaba, alfahari dai da tsoron Allah ne kawai.) HaRiRa mafi girmanku gurin Allah wanda yafi ku tsor-on Allah, haƙiƙa Ubangiji masa-ninc (da zahirinku,) masaninc (da badininku.)

(IMANI CIKAKKE)

14. Larabawan Kauye sukace, (wadansu mutane ne na bani Sa'adu) "mun bada gaskiya da zukatanmu" cene (dasu). "baku bada gaskiya ba, ku dai ce "mun jawu da zahirinmu" har yau imani bai shiga cikin zuka-tanku ba, (saidai ana sauraren zai shiga inkun bi Allah da manzonsa da imani da wanin-sa), bazai tauye muku komai na ladan aikinku ba, haƙiƙa Allah Shine mai gafara (ga muminai) mai rahama (garesu).

إِنَّمَا ٱلْمُؤْمِنُونَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ ثُمَّ لَمْ يَرْتَابُوا۟ وَجَٰهَدُوا۟
بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلصَّٰدِقُونَ ﴿15﴾ قُلْ أَتُعَلِّمُونَ
ٱللَّهَ بِدِينِكُمْ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۚ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿16﴾
يَمُنُّونَ عَلَيْكَ أَنْ أَسْلَمُوا۟ ۖ قُل لَّا تَمُنُّوا۟ عَلَىَّ إِسْلَٰمَكُم ۖ بَلِ ٱللَّهُ
يَمُنُّ عَلَيْكُمْ أَنْ هَدَىٰكُمْ لِلْإِيمَٰنِ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿17﴾
إِنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ غَيْبَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ وَٱللَّهُ بَصِيرٌۢ بِمَا تَعْمَلُونَ ﴿18﴾

50 سُورَةُ قٓ مَكِّيَّة

وَهِيَ خَمْسٌ وَأَرْبَعُونَ ءَايَة 45

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

قٓ ۚ وَٱلْقُرْءَانِ ٱلْمَجِيدِ ﴿1﴾ بَلْ عَجِبُوٓا۟ أَن جَآءَهُم مُّنذِرٌ مِّنْهُمْ فَقَالَ ٱلْكَٰفِرُونَ
هَٰذَا شَىْءٌ عَجِيبٌ ﴿2﴾ أَءِذَا مِتْنَا وَكُنَّا تُرَابًا ۖ ذَٰلِكَ رَجْعٌۢ بَعِيدٌ ﴿3﴾ قَدْ عَلِمْنَا
مَا تَنقُصُ ٱلْأَرْضُ مِنْهُمْ ۖ وَعِندَنَا كِتَٰبٌ حَفِيظٌۢ ﴿4﴾ بَلْ كَذَّبُوا۟ بِٱلْحَقِّ
لَمَّا جَآءَهُمْ فَهُمْ فِىٓ أَمْرٍ مَّرِيجٍ ﴿5﴾ * أَفَلَمْ يَنظُرُوٓا۟ إِلَى ٱلسَّمَآءِ فَوْقَهُمْ
كَيْفَ بَنَيْنَٰهَا وَزَيَّنَّٰهَا وَمَا لَهَا مِن فُرُوجٍ ﴿6﴾ وَٱلْأَرْضَ مَدَدْنَٰهَا وَأَلْقَيْنَا فِيهَا رَوَٰسِىَ
وَأَنۢبَتْنَا فِيهَا مِن كُلِّ زَوْجٍۭ بَهِيجٍ ﴿7﴾ تَبْصِرَةً وَذِكْرَىٰ لِكُلِّ عَبْدٍ مُّنِيبٍ ﴿8﴾

ثمن

15. Dahir muminai dai sune wadanda suka bada gaskiya da Allah da mursalansa sannan basuyikokonto (cikin imaninsu ba), sukayi yaƙi da dukiyoyinsu da kawukansu saboda Allah a cikin sha'anin inganta addinin Allah. WacTancanenka sune ainahin magasgata a cijdn imani (Ban da wadanda sukace "mun bada gaskiya a kan harshe, al-hali ba a sami komai basai za-hirin musulinci a wurinsu).
16. Cene (dasu) "shin kwa dinga sanarwa Allah addininku (a cikin fadinky mun bada gaskiya?) Allah yana sane da abinda ke cikin sammai da ƙassai, kuma Allah masanine da ko-mai.
17. Suna goranta maka cewa sun bada gaskiyaba tare dayaƙi ba, cene "kadaku ,goranta mini mu-suluncinku, bari! Allah ne yake kwa££wara a gareku donya shirye ku izuwa imani, inkun kasance magasgata (a cikin fadinku mun bada gaskiya).
18. Haƙiƙa Ubangiji yasan asirin sammai da ƙassai (ai abinda ya faku a cikinsu). Allah mai ci-kakken sanine a cikin abinda kuke aikatawa, (ba abinda yake buyagareshi).

WANNAN SURA ITACE SURATU KAF
A MAKKA AKA SAUKAR DA ITA. AYA ARBA'IN DA BIYAR CE (45)
Ina farawa dasunan Ubangiji mai jin□an talikai a duniyagaba daya, mai jin□an Muminai a Lahira a kebe

(Wannan sura ta Runshi Tashin Al-kiyama da masu musunsa da saba misalce-misalce da Anna-bawa da al'ummansu dayaya ƙarshensu ya zama da halittar mutum da ƙarshensa da haluluwan Ranar Alƙiyama da Wutada Aljanna da ba'alin ayoyin Allah masu shaidawa da yiwu-war Tashin Alƙiyama, wato ita wanan sura dukkanta ta tattare ne a cikin Tashin Al□iyama da yiwuwa tasa).

(MUSUN TASHIN ALƘIYAMA DA DALILAN YIWUWA TASA)

1. Allahu a'alamu bi muradihi bi zalika, wato Allah ne yasan abinda ake nufi da wannan. Ubangiji yayi rantsuwa cewa kafiran Makka basu bada gaskiya da Manzon Allah sallallahu alaihi wasallama ba).
2. Bari! sun yi mana ki cewa mai gargadi yazo masu daga cikin-su, (yana gargadinu da wuta bayan tashin alKiyana), sai kafi-rai sukace: "Wannan ban tsor-on abu ne mai ban mana ki."
3. Shin idan mun mutu mun zamo turbaya za a komo da mu? Kai wancanenka komowa ne mai nisa da gaske.
4. Haƙiƙa mun san abinda ƙasa take tauyewa daga cikinsu littafi mai kiyaye dukkan lamura yana ga-remu (Shine Lauhil Mahfuzu.)
5. Bari! sun ƙaryatada gaskiya Shine Alƙur'ani yayin dayazo musu, su a cikin sha'anin Anna-bi (Sallallahu alaiki wa sallama) da alƙur'ani suna cikin sha'ani marikici, (wani yayinsukace matsafi ne; wani yayinsukace mawaKi ne, alƙur'ani waka ne,wani lokaci sukace boka ne, alku'ani bokanci ne.)
6. To shin basuyiduba bane da idanuwansu (zamanin da suka musanci tashin alƙiyama) izuwa sama tana burbushinsu? yaya muka gina ta bada ginshiKi ba muka kawata tada taurari, batada wasu tsage-tsage dasuke lai-fintata.
7. (Su basu duba) ƙasa ba,? yaya muka shimfidata a kan fuskar ruwa, muka kafa duwarwatsu a cikinta matabbata, muka tsirar daga cikinta daga dukkan nau'i kyakkyawa.
8. (Mun aikata wannan gare ku) don lurarwa da kuma gargadi ga dukkan bawa mai komowa ga Allah da da'a.

وَنَزَّلْنَا مِنَ السَّمَاءِ مَاءً مُّبَارَكًا فَأَنبَتْنَا بِهِ جَنَّاتٍ وَحَبَّ الْحَصِيدِ ﴿9﴾ وَالنَّخْلَ
بَاسِقَاتٍ لَّهَا طَلْعٌ نَّضِيدٌ ﴿10﴾ رِّزْقًا لِّلْعِبَادِ ۖ وَأَحْيَيْنَا بِهِ بَلْدَةً مَّيْتًا ۚ كَذَٰلِكَ
الْخُرُوجُ ﴿11﴾ كَذَّبَتْ قَبْلَهُمْ قَوْمُ نُوحٍ وَأَصْحَابُ الرَّسِّ وَثَمُودُ ﴿12﴾ وَعَادٌ
وَفِرْعَوْنُ وَإِخْوَانُ لُوطٍ ﴿13﴾ وَأَصْحَابُ الْأَيْكَةِ وَقَوْمُ تُبَّعٍ ۚ كُلٌّ كَذَّبَ الرُّسُلَ
فَحَقَّ وَعِيدِ ﴿14﴾ أَفَعَيِينَا بِالْخَلْقِ الْأَوَّلِ ۚ بَلْ هُمْ فِي لَبْسٍ مِّنْ خَلْقٍ جَدِيدٍ ﴿15﴾ وَلَقَدْ
خَلَقْنَا الْإِنسَانَ وَنَعْلَمُ مَا تُوَسْوِسُ بِهِ نَفْسُهُ ۖ وَنَحْنُ أَقْرَبُ إِلَيْهِ مِنْ حَبْلِ الْوَرِيدِ ﴿16﴾
إِذْ يَتَلَقَّى الْمُتَلَقِّيَانِ عَنِ الْيَمِينِ وَعَنِ الشِّمَالِ قَعِيدٌ ﴿17﴾ مَّا يَلْفِظُ مِن قَوْلٍ إِلَّا
لَدَيْهِ رَقِيبٌ عَتِيدٌ ﴿18﴾ وَجَاءَتْ سَكْرَةُ الْمَوْتِ بِالْحَقِّ ۖ ذَٰلِكَ مَا كُنتَ مِنْهُ تَحِيدُ ﴿19﴾
وَنُفِخَ فِي الصُّورِ ۚ ذَٰلِكَ يَوْمُ الْوَعِيدِ ﴿20﴾ وَجَاءَتْ كُلُّ نَفْسٍ مَّعَهَا سَائِقٌ وَشَهِيدٌ ﴿21﴾
لَّقَدْ كُنتَ فِي غَفْلَةٍ مِّنْ هَٰذَا فَكَشَفْنَا عَنكَ غِطَاءَكَ فَبَصَرُكَ الْيَوْمَ حَدِيدٌ ﴿22﴾ وَقَالَ
قَرِينُهُ هَٰذَا مَا لَدَيَّ عَتِيدٌ ﴿23﴾ أَلْقِيَا فِي جَهَنَّمَ كُلَّ كَفَّارٍ عَنِيدٍ ﴿24﴾ مَّنَّاعٍ لِّلْخَيْرِ مُعْتَدٍ
مُّرِيبٍ ﴿25﴾ الَّذِي جَعَلَ مَعَ اللَّهِ إِلَٰهًا آخَرَ فَأَلْقِيَاهُ فِي الْعَذَابِ الشَّدِيدِ ﴿26﴾ * قَالَ
قَرِينُهُ رَبَّنَا مَا أَطْغَيْتُهُ وَلَٰكِن كَانَ فِي ضَلَالٍ بَعِيدٍ ﴿27﴾ قَالَ لَا تَخْتَصِمُوا لَدَيَّ
وَقَدْ قَدَّمْتُ إِلَيْكُم بِالْوَعِيدِ ﴿28﴾ مَا يُبَدَّلُ الْقَوْلُ لَدَيَّ وَمَا أَنَا بِظَلَّامٍ
لِّلْعَبِيدِ ﴿29﴾ يَوْمَ نَقُولُ لِجَهَنَّمَ هَلِ امْتَلَأْتِ وَتَقُولُ هَلْ مِن مَّزِيدٍ ﴿30﴾

ربع

9. Mun sassaukar da ruwa mai ya-wan albarka daga sama, muka tsuro da gonakai dashi da Kwayar hatsi abin girbewa.
10. Muka tsirar da dabinai halin ka-sancewarsu dogwaye suna da huda mai cToddori.
11. Don azurtawa ga bayi, muka rayagari matacce dashi (ru-wan) kamar da muka raya Rekashashshe dashi, haka nan fitar ku daga kaburbura take (to yayakuke musunsa?).

(IZNA TANA DAGA TA'ADAR MUTANEN DA)

12. Mutanen Annabi Nuhu sun karyata Annabi Nuhu da ma'abota rijiya (dasuke a zaune da itada babbobinsu Hanzalatu dan Safuwana, Ance kuma bashi bane) da Samudu (mutanen Annabi Salihu).
13. Da Adu (mutanen Annabi Hudu) da Fir'auna da'yan uwan Annabi Ludu.
14. Da mutanen Annabi Shu'aibu da mutanen Tubba'u (Sarki ne ko Annabi a Yaman ya kira muta-nensa izuwa musulunci suka Earyatashi) dukkan wacTannan sun karyata manzanni (kamar yadda Kuraishu suka karyata manzon Allah) sai narko ya tab-bata (Shine mukayi azaba a kansu gaba daya. Kada Idrjinka ya yi lomci da kaftrcin kuraishu).
15. Shin yanzu mun gajiya ne da halittar farko? (A'a saboda haka bazamu gaji a maida halitta a marra ta biyu ba), bari! su suna cikin rikici na daga halitta sabu-wa (Shinc tashin alkiyama).

(TSORON ALLAH DA TSORON AZABA RANAR LAHIRA)

16. Hakika mun halicci mutum, mu mun san abinda ransa take was-iwasi dashi, mune mafi kusa izuwa gare sni daga jijiyar wuya, wato majinatai guda biyu.
17. Zamanin da Mala'iku guda biyu masu karbar aiki suke kansa suna zaune a dama da hauni.
18. Baya fada daga wata magana, face mai zaman dirshan yana nan gareshi.
19. Magagin mutuwa tazo masa da gaskiya (daga lamarin lahira, mai musun ta zai ga al'amarin gaskiyar kakara wato Shine wannan tasananin wahala,) wancanenka mutuwa Shine abinda kake gudu daga gareshi.
20. An yi busa a kaho saboda tashin alkiyama, wancanenka busa Shine ranar narko ga kafirai da aza-ba.
21. Kowace rai tazo (mahashar,) Mala'ika mai kare ta yana tareda itada mai shaida (dazai shaida da aikinta, Shine han-naye da kafafuwa.)
22. (Ana fada ga kafiri) "lallai ka kasance a cikin rafkana daga wannan rana da abinda kake gani a yau muka yaye lul-lubinka, to idonka a yau mai kaifin gani ne, (kana riska dashi a yau abinda kayi musu dashi a duniya.)"
23. Abokinsa (wato Mala'ikan da aka wakkala dashi) yace "Wannan Shine abinda yake wurina mahalarci".
24. Sai a ce da Mala'ikan shamakin wuta, "Ku jefa dukkan kafiri mai taurin kai ku jefa shi a Ja-hannama.
25. Mai hana alheri mai hana zakka, azzalumi mai kokonto cikin ad-dininsa.
26. Wanda yasanya abin bautawa daban tareda Allah, to ku jefa shi cikin azaba matsanahciya.
27. Sai abokinsa (shaidan) yace, ya Ubangiji ni ban bashshe shi ba, shiya kasance ne cikin bata mai nisa ga buran gaskiya (na kira shiya amsa mani).
28. Ubangiji yace "kada kuyi gar-dama gare ni na gabatar mukuda azaba a lahira (inbaku bada gaskiya ba).
29. Ba a musanya magana nan gare ni, ni ba mai zalinta ne ga bayi ba.
30. A ranar da yake fada ga Jahan-nama, shin kin cika? Saltace "ba maRara a cikina sai abinda na cika dashi".
31. An kusanta aljanna ga masu tsoron Allah, banesa dasu ba.

وَأُزْلِفَتِ الْجَنَّةُ لِلْمُتَّقِينَ غَيْرَ بَعِيدٍ (31) هَٰذَا مَا تُوعَدُونَ لِكُلِّ أَوَّابٍ حَفِيظٍ (32) مَنْ خَشِيَ
الرَّحْمَٰنَ بِالْغَيْبِ وَجَاءَ بِقَلْبٍ مُنِيبٍ (33) ادْخُلُوهَا بِسَلَامٍ ذَٰلِكَ يَوْمُ الْخُلُودِ (34) لَهُم
مَا يَشَاءُونَ فِيهَا وَلَدَيْنَا مَزِيدٌ (35) وَكَمْ أَهْلَكْنَا قَبْلَهُم مِّن قَرْنٍ هُمْ أَشَدُّ مِنْهُم بَطْشًا
فَنَقَّبُوا فِي الْبِلَادِ هَلْ مِن مَّحِيصٍ (36) إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَذِكْرَىٰ لِمَن كَانَ لَهُ قَلْبٌ
أَوْ أَلْقَى السَّمْعَ وَهُوَ شَهِيدٌ (37) وَلَقَدْ خَلَقْنَا السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا فِي سِتَّةِ
أَيَّامٍ وَمَا مَسَّنَا مِن لُّغُوبٍ (38) فَاصْبِرْ عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَسَبِّحْ بِحَمْدِ رَبِّكَ قَبْلَ طُلُوعِ
الشَّمْسِ وَقَبْلَ الْغُرُوبِ (39) وَمِنَ اللَّيْلِ فَسَبِّحْهُ وَإِدْبَارَ السُّجُودِ (40) وَاسْتَمِعْ يَوْمَ يُنَادِ
الْمُنَادِ مِن مَّكَانٍ قَرِيبٍ (41) يَوْمَ يَسْمَعُونَ الصَّيْحَةَ بِالْحَقِّ ذَٰلِكَ يَوْمُ الْخُرُوجِ (42) إِنَّا نَحْنُ
نُحْيِي وَنُمِيتُ وَإِلَيْنَا الْمَصِيرُ (43) يَوْمَ تَشَقَّقُ الْأَرْضُ عَنْهُمْ سِرَاعًا ذَٰلِكَ حَشْرٌ عَلَيْنَا
يَسِيرٌ (44) نَحْنُ أَعْلَمُ بِمَا يَقُولُونَ وَمَا أَنتَ عَلَيْهِم بِجَبَّارٍ فَذَكِّرْ بِالْقُرْآنِ مَن يَخَافُ وَعِيدِ (45)

51 سُورَةُ الذَّارِيَاتِ مَكِّيَّةٌ
وَهِيَ سِتُّونَ آيَةً 60

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

ثمن

* وَالذَّارِيَاتِ ذَرْوًا (1) فَالْحَامِلَاتِ وِقْرًا (2) فَالْجَارِيَاتِ يُسْرًا (3)
فَالْمُقَسِّمَاتِ أَمْرًا (4) إِنَّمَا تُوعَدُونَ لَصَادِقٌ (5) وَإِنَّ الدِّينَ لَوَاقِعٌ (6)

32. Za a ce dasu, "wannan abin ga-nin nan abinda ake muku alkawari dashi, ga dukkan mai komawa da al'amarinsa izuwa Allah, mai kiyayewa iyakokin Allah".
33. "Wanda yaji tsoron Ubangiji yazoda zuciya mai gabata izuwa da'ar Ubangiji, "ana fada ga masu tsoron Ubangiji."
34. "Ku shigeta lafiya sumul, wan-canenka rana ce ta dauwama (a cikin aljanna)."
35. Abinda suke so na garesu, mu kuma ƙari yana garemu (kan abinda suka aikatada wanda suka nema).

(BAN TSORO GA MASU MUSUN ALƘIYAMA)

36. Haƙiƙa da yawa muka halakar gaban kafiran kuraishu na daga tsaratsaran dasuke sune mafi tsananin karfi daga garesu na kafirai, sukabincika a garuru-wa, yalla akwai wata mak-arcTada garesu da zata hana musu mutuwa? (Basu samu ba).
37. Haƙiƙa akwai gargaɗi cikin wancanenka abin anbato ga wanda hankali ya kasance gareshi, ko ya karkata kunnensa, shi yana mai shaidawa a zuciyarsa.
38. Haƙiƙa mun halicci sammai da ƙassaida abinda ke cikinsu cikin milcdarin kwana shida, ga-jiyabata same mu ba. (Wannan aya ta sauka ne don raddi ga Yahudu a cikin faɗinsu " haƙiƙa Ubangiji ya huta ranar Asabar", don koruwar wahala ga buransa, don kuma tsarkakarsa ga buran sifar talikai, kuma da rashin shafefeniya tsakaninsa da tsaka-nin waninsa domin aikinsa bada gabobi bane).
39. Daure (ya Annabi Sallallahu alaika wa sallama) bisa abinda suke faɗa (maka da waninsa na daga kamantawa da ƙaryatawa,) kayi tasbihi da godiyar Ubangijinka (wato' yi Salla kana mai godiya) gaban hudowar rana;
(sallar Asuba) sannan da bayan faduwarta (wato sallar Azahar daLa'asar.)

(AURADU DA AZKARU BAYAN KOWACE SALLA)

40. Da daddare kuma kayi sallah gareshi da bayan sujadodi na farillai, (Ance tasbihi tareda go-diya a cikin waɗannan lokutan, ba shakka Auradu da Azkaru waɗanda manzon Allah Sallalla-hu alaihi wa sallama ya aiyana-su suna daga cikin umarnin wannan aya, haka ma Auradu da Azkaru waɗanda Auliya'u suka aiyana, kamar wurdi AH-LIDDARI wanda SHEHU ABDUL-KADIR JILANI ya aiyanasu Allah ya kara masa yardasu ma suna daga cikin wannan aya).
41. Ka saurari ranar da mai kira yake kira (ya kai abokin zance) daga guri makusanci (daga sama Shine fa ta Baitul Mukaddisi yafi kusanci da sama izuwa ƙasa. Yana cewa Yake wannan Kasusuwa tsofaffi, ya ke waɗannan jijiyoyi waɗanda suka yanyanke, Yake waɗannan namomi wacce ta kerkece, Yake waɗannan gasu waɗanda sukayi dabam-dabam,Ubangiji yana umarninku saboda hukunci).
42. Ranar da talikai suke jin tsawa da gaskiya (ta tashin alfdyama Itace busa ta biyu, daga Israfi-la) wancanenka rana Shine ra-nar fita (daga kaburbura.)
43 Haƙiƙa mu mune muke rayawa mu ke matarwa, izuwa garemu kowa zai koma.
44. Ranar da ƙasa take kekkecewa saboda buransu suna gaggawa, wancanenka tarawa ne mai sau-ki a gare mu.
45. Mune masana da abinda suke facTe (su kafiran Kuraishu) kai ba mai tilasta bane a kansu (da zaka tilashe su, wannan ya ka-sance ne tun kafin umarni dayaƙi). Kayi gargaɗi da Kur'ani ga wanda yake tsoron narkona (sune Muminai.)

Wannan sura Itace Suratu Zariyad

A Makka aka saukar da ita. Aya sitdn ce (60)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinSan Muminai a Lahiraa keɓe

(Wannan sura ta ƙunshi Tashin Alƙiyama da rantsuwa a kansa da anbaton ba'alin haluluwan Muminai tareda kafirai, sannan Kissoshin ba'alin Annabawa daƙissar Adu da Samudu, da mu-tanen Annabi Nuhu da Tauhidi da bayanin dabi' o'in mutane).

1. Ubangiji ya rantse da iskoki masu shekad da turbaya da waninsa sheƙarwa.

وَالسَّمَآءِ ذَاتِ الْحُبُكِ ﴿7﴾ إِنَّكُمْ لَفِي قَوْلٖ مُّخْتَلِفٖ ﴿8﴾ يُوفَكُ عَنْهُ
مَنْ اُفِكَ ﴿9﴾ قُتِلَ الْخَرَّاصُونَ ﴿10﴾ الَّذِينَ هُمْ فِي غَمْرَةٖ سَاهُونَ ﴿11﴾
يَسْـَٔلُونَ أَيَّانَ يَوْمُ الدِّينِ ﴿12﴾ يَوْمَ هُمْ عَلَى النَّارِ يُفْتَنُونَ ﴿13﴾
ذُوقُواْ فِتْنَتَكُمْ هَٰذَا الَّذِي كُنتُم بِهِۦ تَسْتَعْجِلُونَ ﴿14﴾ إِنَّ الْمُتَّقِينَ
فِي جَنَّٰتٖ وَعُيُونٍ ﴿15﴾ ءَاخِذِينَ مَا ءَاتَىٰهُمْ رَبُّهُمْ إِنَّهُمْ كَانُواْ قَبْلَ
ذَٰلِكَ مُحْسِنِينَ ﴿16﴾ كَانُواْ قَلِيلاٗ مِّنَ الَّيْلِ مَا يَهْجَعُونَ ﴿17﴾ وَبِالْأَسْحَارِ
هُمْ يَسْتَغْفِرُونَ ﴿18﴾ وَفِي أَمْوَالِهِمْ حَقّٞ لِّلسَّآئِلِ وَالْمَحْرُومِ ﴿19﴾
وَفِي الْأَرْضِ ءَايَٰتٞ لِّلْمُوقِنِينَ ﴿20﴾ وَفِي أَنفُسِكُمْ أَفَلَا تُبْصِرُونَ ﴿21﴾
وَفِي السَّمَآءِ رِزْقُكُمْ وَمَا تُوعَدُونَ ﴿22﴾ فَوَرَبِّ السَّمَآءِ وَالْأَرْضِ إِنَّهُ لَحَقّٞ
مِّثْلَ مَا أَنَّكُمْ تَنطِقُونَ ﴿23﴾ هَلْ أَتَىٰكَ حَدِيثُ ضَيْفِ إِبْرَٰهِيمَ الْمُكْرَمِينَ ﴿24﴾
إِذْ دَخَلُواْ عَلَيْهِ فَقَالُواْ سَلَٰماٗ قَالَ سَلَٰمٞ قَوْمٞ مُّنكَرُونَ ﴿25﴾ فَرَاغَ
إِلَىٰ أَهْلِهِۦ فَجَآءَ بِعِجْلٖ سَمِينٖ ﴿26﴾ فَقَرَّبَهُۥ إِلَيْهِمْ قَالَ أَلَا
تَاكُلُونَ ﴿27﴾ فَأَوْجَسَ مِنْهُمْ خِيفَةٗ قَالُواْ لَا تَخَفْ وَبَشَّرُوهُ بِغُلَٰمٍ
عَلِيمٖ ﴿28﴾ فَأَقْبَلَتِ امْرَأَتُهُۥ فِي صَرَّةٖ فَصَكَّتْ وَجْهَهَا وَقَالَتْ عَجُوزٌ
عَقِيمٞ ﴿29﴾ قَالُواْ كَذَٰلِكِ قَالَ رَبُّكِ إِنَّهُۥ هُوَ الْحَكِيمُ الْعَلِيمُ ﴿30﴾

2. Kuma da giza-gizai masu dauka-ka ruwa mai nauyi nitu-niƙi.
3. Ya rantse da jiraga masu dauka sauwaRe.
4. Kana Mala'iku masu raba arzuka da ruwaiwai da waninta, tsakanm bayi da garuruwa.
5. Dahir abinda akc muku alkawari dashi (na tashin Alkiya da wa-ninsa) lallai gaskiya ne.
6. Kunia haƙiƙa sakamako (bayan hisabi) lallai gaskiya ne, (ba kokonto cikinsa.)
7. Ubangiji yayi rantsuwa da sama ma'abociyar hanyoyi, (na zahi-n, kamar na taurari da Mala'iku, dana badini, kamar hanyoyın kafa dalili izuwa sanın Ubangiji.)
8. Haƙiƙa (yaku mutanen Makka, a sha'anin Annabi Sallallahu alaihi wa sallama da alƙur'ani,) lallai kuna cikin magana mai sassabawa, (Ance mawaki ne, Ance matsafi ne, Ance boka ne, alƙur'ani waƙa ne, tsafi ne, bo-kanci ne).
9. Ana juyar wa ga buran Alƙur'ani wanda aka juyad dashi (daga hanyar shiriya a cikin sanin Allah).
10. An la'anci maƙaryata ma'abota magana mai sassabawa.
11. Waɗanda sukc marafkana (ga buran al'amarin lahira) suna cikin magagi.
12. Suna tambayar (Annabi Sallalla-hu alaihi wa sallama tanbayon izgili) yaushe ne ranar sakamo? (jawabinsa tana zuwa).
13. Ranar dasu ake musu azaba a kan wuta.
14. (Ana ce dasu ranar azaban nan) "Ku ɗanɗani azabarku wannan azabtawa, Shine wanda kuka kasance kuna neman gaggawa tasa cikin afkuwarta don izgili ."

(SU WAYE MASU TSORON ALLAH? ME YE SAKAMAKONSU?)

15. Haƙiƙa masu tsoron Allah suna cikin aljannatai da mana ko (wato idandunan ruwa.)
16. Suna masu karbar abinda Ubangiji ya basu (na daga sakamako,) haƙiƙa su sun kasance ga-ban wancanenka (wato shiga aljanna) masu kyakkyawan aiki ne (a duniya.)
17. Sun kasance kaɗan ne Kwarai suke bacci da daddare, (suna ta sallah da ibada a cikin mafi ya-wan dare).
18. A lokatan sahur, su suna neman gafarar Ubangiji suna cewa (Allahumma ifgir lana).
19. Akwai haKId cikin dukiyoyinsu ga mai bara, da wanda baya bara saboda kamun kai.
20. Akwai ayoyi (masu nuna girman Allah) a cikin ƙasa (na duwar-watsu da koguna da itatuwa da tsirraı da da Annabawa da Wa-liyai da Salihai da waninsu) ga masu sakankancewa (da Allah).
21. Akwai ayoyi har yau a cikin kawukanku, (tun daga farin halittarku izuwa karewarku.) Shin to bakuyi tunani bane (a cikin wancanenka ku kafa dalili dashi, a bisa girman mahaliccin-ku?).
22. Arzikinku yana cikin sama (wato ruwa wandaShine tsiri daya kasantu daga gareshi, wandaShine arzikin) da abinda ake muku alwashi dashi (na a£uba, ai yana mbuce a sama.)
23. To na rantse da Ubangijin sam-mai da ƙassai: haƙiƙa abinda ake muku alwashi lallai gaskiya ne. Misalin furucinku (a cikin tabbatarwarsa cewa maganarku ce.)

(GIRMAMA WAN ALLAH DA WALIYANSA DA WULAƘANTAWARSA GA MAGAUTANSA)

24. Labarin baƙin Annabi Ibrahimu ababan girmama wa yazo maka? (Mala'ikune guda goma sha biyu, Mala'ika Jibrilu yana cikinsu).
25. Zamanin da suka shiga gareshi sukace "gaisuwa", (wato muna gaisheka gaisuwa), yace; "gai-suwa, ku mutane ne? Bamu san ku ba".
26. Saiya surare izuwa iyalinsa a asirce, sai yazo da, ɗan maraRi mai Idba soyayye.
27. Sai yakusantashi izuwa garesu yace: "ba kwaci ba? (Basu amsa ba.)
28. Saiya ɓoye tsoronsu a cikin ran-sa sai sukace "kada kaji tsoro, mu jakadun Ubangijinka ne" Sukayi masa albishir dayaro mai ilimi, (Ancc IshaKunc tam-far da aka anbata cikin Surutu Hudin).
29. Sai matatasa ta gabato (Itace Saratu) a cikin hayaniya ta kant-same fuskartada mari, Tace "ni tsohuwa ce bakarara (bata taɓa haihuwa badadai ranta shekara dari ɗaya, ran Annabi Ibrahimu kuma shekara dari, ko ransa shekara dari da ishirin, ranta kuma shekara casa'in).
30. Sukace: ("Kamar faɗinmu a cikin bishara) Ubangijinki yace; haƙiƙa Shine gwani (cikin ai-kinsa) masani da (halitta).

حزب

*قَالَ فَمَا خَطْبُكُمْ اَيُّهَا الْمُرْسَلُوْنَ ﴿31﴾ قَالُوْٓا اِنَّآ اُرْسِلْنَآ اِلٰى قَوْمٍ
مُّجْرِمِيْنَ ﴿32﴾ لِنُرْسِلَ عَلَيْهِمْ حِجَارَةً مِّنْ طِيْنٍ ﴿33﴾ مُّسَوَّمَةً عِنْدَ رَبِّكَ
لِلْمُسْرِفِيْنَ ﴿34﴾ فَاَخْرَجْنَا مَنْ كَانَ فِيْهَا مِنَ الْمُؤْمِنِيْنَ ﴿35﴾ فَمَا وَجَدْنَا فِيْهَا
غَيْرَ بَيْتٍ مِّنَ الْمُسْلِمِيْنَ ﴿36﴾ وَتَرَكْنَا فِيْهَآ اٰيَةً لِّلَّذِيْنَ يَخَافُوْنَ الْعَذَابَ
الْاَلِيْمَ ﴿37﴾ وَفِيْ مُوْسٰٓى اِذْ اَرْسَلْنٰهُ اِلٰى فِرْعَوْنَ بِسُلْطٰنٍ مُّبِيْنٍ ﴿38﴾
فَتَوَلّٰى بِرُكْنِهٖ وَقَالَ سٰحِرٌ اَوْ مَجْنُوْنٌ ﴿39﴾ فَاَخَذْنٰهُ وَجُنُوْدَهٗ
فَنَبَذْنٰهُمْ فِى الْيَمِّ وَهُوَ مُلِيْمٌ ﴿40﴾ وَفِيْ عَادٍ اِذْ اَرْسَلْنَا عَلَيْهِمُ الرِّيْحَ
الْعَقِيْمَ ﴿41﴾ مَا تَذَرُ مِنْ شَيْءٍ اَتَتْ عَلَيْهِ اِلَّا جَعَلَتْهُ كَالرَّمِيْمِ ﴿42﴾
وَفِيْ ثَمُوْدَ اِذْ قِيْلَ لَهُمْ تَمَتَّعُوْا حَتّٰى حِيْنٍ ﴿43﴾ فَعَتَوْا عَنْ اَمْرِ رَبِّهِمْ
فَاَخَذَتْهُمُ الصّٰعِقَةُ وَهُمْ يَنْظُرُوْنَ ﴿44﴾ فَمَا اسْتَطَاعُوْا مِنْ قِيَامٍ
وَّمَا كَانُوْا مُنْتَصِرِيْنَ ﴿45﴾ وَقَوْمَ نُوْحٍ مِّنْ قَبْلُ اِنَّهُمْ كَانُوْا قَوْمًا فٰسِقِيْنَ ﴿46﴾
وَالسَّمَآءَ بَنَيْنٰهَا بِاَيْىدٍ وَّاِنَّا لَمُوْسِعُوْنَ ﴿47﴾ وَالْاَرْضَ فَرَشْنٰهَا
فَنِعْمَ الْمٰهِدُوْنَ ﴿48﴾ وَمِنْ كُلِّ شَيْءٍ خَلَقْنَا زَوْجَيْنِ لَعَلَّكُمْ
تَذَكَّرُوْنَ ﴿49﴾ فَفِرُّوْٓا اِلَى اللّٰهِ اِنِّيْ لَكُمْ مِّنْهُ نَذِيْرٌ مُّبِيْنٌ ﴿50﴾
وَلَا تَجْعَلُوْا مَعَ اللّٰهِ اِلٰهًا اٰخَرَ اِنِّيْ لَكُمْ مِّنْهُ نَذِيْرٌ مُّبِيْنٌ ﴿51﴾

31. Yace "Mene? ne sha'aninku yaku wađannan jakadu?".
32. Sukace: " Haƙiƙa mu an aiko mu izuwa mutane masu laifi (kafirai mutanen Annabi Luđu).
33. "Don mu sako musu duwatsu a kansu na wuta.
34. Wacce akayi mata alama da wandaza a jefa da ita nan ga Ubangijinka ga masu ɓarna (zailcewa mazaje tareda kafircinsu)".
35. Muka fitar da wanda ya kasance a cikinsu (wato al'umar Annabi Luđu), na daga muminai (saboda halakad da kafirai).
36. To bamu sami komai a cikinta basai daki đaya na daga musul-mi, (sune Annabi Luđu da 'ya'yansa guda biyu, mata, an kamanta su da imani da musu-lunci, ai sun gasgatada zukatan-su, suna aikata aiyuka da gabubbansu.)
37. Muka sanya aya a cikinta ga wađanda suke tsoron azaba mai rac fađi.

(IYAKAR MASU SHISHSHIGI DA MASU ƘARYATAWA)

38. Mun sanya izna a cikin ƙissar Annabi Musa (alaihissalamu) zamanin da muka aiko shi izu-wa Fir'auna yana tareda hujja mabaiyaniya.
39. Saiya bijire ga buran imani tareda rundunarsa, yace (da Annabi Musa shi) matsafi ne, ko maras hankali.
40. Sai muka danƙa shi da rundu-narsa, sai muka jefa su a cikin kogi, alhali shi Fir'aunu ya aika abindaza a zarge shi a kansa, (Shine ƙaryata manzanni da da'awar Allantaka).
41. Mun sanya aya cikin halakad da Adawa, zamanin da muka sako iska bakarara a kansu (wato Itace wacce babu alheri a cikinta saboda bata dauke da ruwa, bata buran bishiyoyi Itace ake ce da ita daburu).
42. Bata barin daga wani abu (rai ko dukiya) data wuce a kansa, face ta maidashi kamar dan-daƙa £(cen 'abu.
43. Mun sanya aya cikin halakad da Samudawa, zamanin da akace (dasu bayan sare taguwa), "ku more dadi har izuwa lokacin ajalinku, (gwargwadon kwana uku).
44. Sai sukayi ginnan kai ga buran bin umarnin Ubangijinsu, sai kururuwa mai halalkarwa ta dankesu, alhali suna kallon (abindazai sauka a garesu).
45. Basu sami damar miKewa (zam-anin saukar azabar nan ba), basu kasance masu intikami (a bisa wanda ya halakar dasu ba, wato azabtarwa).
46. Mun halakar da mutanen Anna-bi Nuhu tun gaban wađannan abadan anbato, haƙiƙa su sun kasance mutane fasiƙai.

(WANI ABU DAGA AYOYIN ALLAH NA FILIN DUNIYA)

47. Mun gina sama da Karfi, haƙiƙa mu masu ikone.
48. ƙasa mun shimifidata, madallar masu shimfidawa mu.
49. Daga kowane abu mun halicci nau'o'i bibiyu (kamar namiji da mace, sama da ƙasa, rana da wata, ƙasa mai taushi da dutse, damina da dari, zaƙi da tsami da haske da duhu) don ku wa'azantu, ku san cewa maha-liccin wađannan nau'o'i đaya ne tal ku bauta masa).
50. Cene dasu "Ku girka a guje izu-wa Allah, haƙiƙa ni mai girgacTi ne mabaiyanin gargađi ").
51. Kadaku ,sanya wani Ubangiji tareda Allah ni mai gargađi ne mabaiyanin gargađi ne daga Allah.

كَذَٰلِكَ مَآ أَتَى ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِم مِّن رَّسُولٍ إِلَّا قَالُواْ سَاحِرٌ
أَوْ مَجْنُونٌ ﴿52﴾ أَتَوَاصَوْاْ بِهِۦۚ بَلْ هُمْ قَوْمٌ طَاغُونَ ﴿53﴾ فَتَوَلَّ عَنْهُمْ
فَمَآ أَنتَ بِمَلُومٍ ﴿54﴾ وَذَكِّرْ فَإِنَّ ٱلذِّكْرَىٰ تَنفَعُ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿55﴾
* وَمَا خَلَقْتُ ٱلْجِنَّ وَٱلْإِنسَ إِلَّا لِيَعْبُدُونِ ﴿56﴾ مَآ أُرِيدُ مِنْهُم
مِّن رِّزْقٍ وَمَآ أُرِيدُ أَن يُطْعِمُونِ ﴿57﴾ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلرَّزَّاقُ
ذُو ٱلْقُوَّةِ ٱلْمَتِينُ ﴿58﴾ فَإِنَّ لِلَّذِينَ ظَلَمُواْ ذَنُوبًا مِّثْلَ ذَنُوبِ أَصْحَٰبِهِمْ
فَلَا يَسْتَعْجِلُونِ ﴿59﴾ فَوَيْلٌ لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن يَوْمِهِمُ ٱلَّذِي يُوعَدُونَ ﴿60﴾

ثمن

52 سُورَةُ الطُّورِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ سَبْعٌ وَأَرْبَعُونَ ءَايَةً 47

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلطُّورِ ﴿1﴾ وَكِتَٰبٍ مَّسْطُورٍ ﴿2﴾ فِي رَقٍّ مَّنشُورٍ ﴿3﴾ وَٱلْبَيْتِ ٱلْمَعْمُورِ
وَٱلسَّقْفِ ٱلْمَرْفُوعِ ﴿4﴾ وَٱلْبَحْرِ ٱلْمَسْجُورِ ﴿5﴾ إِنَّ عَذَابَ رَبِّكَ لَوَٰقِعٌ ﴿6﴾ مَّا لَهُۥ مِن
دَافِعٍ ﴿7﴾ يَوْمَ تَمُورُ ٱلسَّمَآءُ مَوْرًا ﴿8﴾ وَتَسِيرُ ٱلْجِبَالُ سَيْرًا ﴿9﴾ فَوَيْلٌ يَوْمَئِذٍ
لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿10﴾ ٱلَّذِينَ هُمْ فِي خَوْضٍ يَلْعَبُونَ ﴿11﴾ يَوْمَ يُدَعُّونَ إِلَىٰ
نَارِ جَهَنَّمَ دَعًّا هَٰذِهِ ٱلنَّارُ ٱلَّتِي كُنتُم بِهَا تُكَذِّبُونَ ﴿12﴾ ...

52. Kamar wancanenka ne, wani manzo a gabansu bai zo musu ba, face sunce "matsafi ne, ko taɓaɓɓe").
53. Shin wasiyya sukayi da wannan magana dukkansu? (A'a,) bari! Sudai mutane ne masu shishshi-gi (shishshiginsune ya tattara su a kan wannan magana).
54. To rabu dasu kai ba abin zargi bane (saboda ka iyar musu da aike).
55. Kayi gargaɗi da Alƙur'ani gar-gadi tana anfani ga muminai, (wanda Allah yasan cewa zai bada gaskiya).
56. Ban halicci aljanu da mutane ba, sai donsu bauta mini.
57. Ban na nufin wani azurtawa daga garesu izuwa gare ni (wala ga kawukansu wala waninsu), bana nutin su ciyar dani (wala kansu, wala waninsu).
58. Haƙiƙa Ubangiji Shine mai ar-zurtawa, Shine mai ƙarfin badlni.
59. Haƙiƙa waɗanda suka zalinci kansu (da kafirci na mutanen Makka da waninsu) suna da rabo na azaba misalin abokansu (ai misalin waɗanda suke ga-bansu,) su daina garaje (na aza-ba, in mun jinkirtar dasu izuwa ranar aUayama).
60. Azabata tabbata ga waɗanda suka kafirta a cikin ranarsu wacce ake musu alwashi'dashi.

Wannan sura Itace Suratul Duri

a Makka aka saukar da ita. Aya arba'in da bakwai ce (47)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai Jinkan talikai a duniyagaba ɗaya, maijinkan Muminai a Lahira a keɓe

(Wannan sura tayi magana a kan ta-shin alƙiyama da abinda yake cikinsa, da sifar kafirai da mu-minai ranar alƙiyama, da zance da mushurukai da munakasha dasu, wato bincike a cikin akidodinsu batattu da nasihohi da ma'aiki Sallallhu alaihi wa sallama da munafiƙai da kiransu izuwa Allah).

(RANAR ALƘIYAMA DA KAFIRAI A CIKINSA)

1. Ubangiji yayi rantsuwa da dutse (wanda yayi zance da Annabi Musa a kansa), da littafi abin ru-butawa.
2. A cikin fata abin budewa (wato budadcTiyar takarda Attaura ko Alƙur'ani).
3. Da daki abin rayawa (da masu ziyara a sama ta bakwai daura da ƙa 'aba (ana anbatonsa Dura-hu Mala'ika 70.000 suna ziyara tasa a kowace rana suna Dawafi suna Sallah, bazasu komo izu-wa gareshi ba har abada, Ance kuma Shine Ka'aba, ana raya shi da Alhazai da masu ziyara gareshi kowace shekara da kowace rana).

(BAITUL MA'AMURU ABIN RAYAWA NA SAMA DANA ƘASA)

4. Da rufi abindaukakewa (Shine sama).
5. Da kogi abin cikawa da ruwa, (Shine Baharul muhidu).
6. Haƙiƙa azabar Ubangijinka mai afkuwa ce (ga wanda ya cancan-ta).
7. Ba mai ijewa gareshi.
8. Ranar da sama da take juyawa juyawa.
9. Duwatsu suke tafiya tafiya, ta zama ƙura abar shelcewa (don a tabbatacewa baza a komo izu-wa duniya ba).
10. Azaba a wannan rana ta tabbata ga waɗanda basu bada gaskiya (da Annabawa ba).
11. Waɗandasu suke cikin kutsawa suna wasanni.
12. Ranar da ake angizasu izuwa wutar jahannama angizawa, ake cewa dasu (don ururtawa;) wannan Itace wuta wacce kuka kasance kuna ƙaryatawa da ita.

أَفَسِحْرٌ هَٰذَآ أَمْ أَنتُمْ لَا تُبْصِرُونَ ﴿13﴾ اِصْلَوْهَا فَاصْبِرُوٓاْ
أَوْ لَا تَصْبِرُواْ سَوَآءٌ عَلَيْكُمْ إِنَّمَا تُجْزَوْنَ مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿14﴾
إِنَّ ٱلْمُتَّقِينَ فِي جَنَّٰتٍ وَنَعِيمٍ ﴿15﴾ فَٰكِهِينَ بِمَآ ءَاتَىٰهُمْ رَبُّهُمْ
وَوَقَىٰهُمْ رَبُّهُمْ عَذَابَ ٱلْجَحِيمِ ﴿16﴾ كُلُواْ وَاشْرَبُواْ هَنِيٓـًٔا بِمَا كُنتُمْ
تَعْمَلُونَ ﴿17﴾ مُتَّكِـِٔينَ عَلَىٰ سُرُرٍ مَّصْفُوفَةٍ وَزَوَّجْنَٰهُم بِحُورٍ عِينٍ ﴿18﴾
وَالَّذِينَ ءَامَنُواْ وَاتَّبَعَتْهُمْ ذُرِّيَّتُهُم بِإِيمَٰنٍ أَلْحَقْنَا بِهِمْ ذُرِّيَّٰتِهِمْ
وَمَآ أَلَتْنَٰهُم مِّنْ عَمَلِهِم مِّن شَيْءٍ كُلُّ امْرِئٍ بِمَا كَسَبَ رَهِينٌ ﴿19﴾
وَأَمْدَدْنَٰهُم بِفَٰكِهَةٍ وَلَحْمٍ مِّمَّا يَشْتَهُونَ ﴿20﴾ يَتَنَٰزَعُونَ فِيهَا
كَأْسًا لَّا لَغْوٌ فِيهَا وَلَا تَأْثِيمٌ ﴿21﴾ * وَيَطُوفُ عَلَيْهِمْ غِلْمَانٌ ربع
لَّهُمْ كَأَنَّهُمْ لُؤْلُؤٌ مَّكْنُونٌ ﴿22﴾ وَأَقْبَلَ بَعْضُهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ
يَتَسَآءَلُونَ ﴿23﴾ قَالُوٓاْ إِنَّا كُنَّا قَبْلُ فِي أَهْلِنَا مُشْفِقِينَ ﴿24﴾
فَمَنَّ ٱللَّهُ عَلَيْنَا وَوَقَىٰنَا عَذَابَ ٱلسَّمُومِ ﴿25﴾ إِنَّا كُنَّا مِن قَبْلُ
نَدْعُوهُ أَنَّهُ هُوَ ٱلْبَرُّ ٱلرَّحِيمُ ﴿26﴾ فَذَكِّرْ فَمَآ أَنتَ بِنِعْمَتِ رَبِّكَ
بِكَاهِنٍ وَلَا مَجْنُونٍ ﴿27﴾ أَمْ يَقُولُونَ شَاعِرٌ نَّتَرَبَّصُ بِهِۦ رَيْبَ
ٱلْمَنُونِ ﴿28﴾ قُلْ تَرَبَّصُواْ فَإِنِّي مَعَكُم مِّنَ ٱلْمُتَرَبِّصِينَ ﴿29﴾

13. To yanzu wannan azabada kuka gani sihiri ne? (Don kun ce wa-hayi sihiri ne) to ko bakwa gani ne?

14. Ku shigeta, ku (fandani kudarta na zafinta, ku daure ko kadaku ,daure, du ɗaya ne gare ku, do-min haKurin ku bazai anfane ku ba, ana saka muku abinda kuka aikata ne.

(Masu tsoron Allah da sakamakonsu ranar alƙiyama)

15. Haƙiƙa masu jin tsoron Allah suna cikin aljannatai da jin dadi.

16. Suna masu morewar daɗi saboda baiwar da Allah yayi musu da kiyasarwar Ubangijinsu yayi azabar Jahannama.

17. Ana ce dasu: "Kuci ku sha a cikin farin ciki saboda kyakkya-wan aikin da kuka aikata".

18. Suna masu dogaro, a kan gadaje ababan jerawa, munyi musu aure da 'yan matan aljanna, masu yalwar tsagar ido, masu gadagadan idanuwa, wato masu farin ido kamar madara; mun hadasu dasu. (TASIRIN SALIHAI A CIKIN MABIYANSU)

19. Waɗanda suka bada gaskiya, mukabiyar musu da zumyoyin-su (KanKanana da manya) saboda imani na manyan da iyayen a cikin KanKanan, mun riskas da zurriyarsu dasu a cikin aljanna zasu kasance a cikin daraja ta su koda ba' suyiaiki da aikinsu ba don girmama wa ga iyayen saboda tattarar 'ya'yayen zuwa garesu, Sawi yace kamar alma-jirai wato wuridai haƙiƙa ana riskar dasu ga Shehunansu; Shehunan sunna kuma ana risk-ar dasu ga Shehunan in sun ka-sance koma baya dasu a cikin aiki, asali a cikin wannan maga-nar manzon Allah Sallallahu alaihi wa sallama, idan 'yan al-janna suka shiga aljanna, sai dayansu yayi tambayaga iyay-ensa da matarsa da dansa, sai a ce basu riski abinda ka riska ba, sai yace Ya Rabbi, ni nayi aiki ne sabodani dasu, sai ayi umarni da riskar dasu dashi, Sawi). Bamu tauye masu koda hikunnan daga aikinsu ba a kan aikin 'ya'yaye ba, kowane mu-tum abin jinginawa ne da abinda ya aikata na hairi ko sharri.

20. Mun kare su a cikin lokaci bay-an lokaci da abin marmari da nama na daga abinda suke mar-mari koda basu ce a kawo shi ba.

21. Suna miKeKeniyar gidauniya a cikin aljanna basambatu cikinta, ba zunubi (dazai riske su sabanin giyar duniya).

22. Magudantansu zasu dinga ke-wayo a garesu saboda hidima a cikin aljanna; kai kace lu'ulu'i ne abin kiyayewa a cikin kwas-fa (saboda yafi kyau a cikin kwasfarsa).

23. Ba'alinsu yagabata a cikin ba'ali suna tambayar juna (ga abinda suke kansa, da abinda suka sadu izuwa gareshi don jin dadi da furuci da ni'imar UbangiJi).

24. Sukace: (wato suna nuna dalilin saduwarsu da wannan alheri,) haƙiƙa mun kasance muna jin tsoron azabar Ubangiji da iya-linmu a duniya.

25. To Ubangiji yayi baiwa garemu da gafara, ya kiyashe mu azabar wuta, wacce take shiga kafafen gashi.

26. Suka dbre cewa, haƙiƙa mun ka-sance tun gaba a duniya, muna bauta masa, muna kadaitashi, haƙiƙa Ubangiji Shine mana-garci (mai gaskiya cikin alkaw-arinsa) mai girman rahama.

(MUNAKASHA DA MUSHURUKAI DA RUDURE-ƘUDURENSU DA CIKA SURA DA UMARNI DA HAƘURI GA HUKUNCIN ALLAH)

27. Ka dauwama kan gargaɗin (mushurukai, karka daina shi saboda sun a cewa da kai: "Boka, taɓaɓɓe"), to kai ba boka ne ba, ba taɓaɓɓe ne ba, saboda ni'imar da Allah yayi a gareka.

28. Bari! suna cewa shi mawaKi ne, muna sauraron masibun zamani dashi, (ya halaka kamar da wa-ninsa ya halaka na daga guma-ka).

29. Cene "Ku saurari halakata, ni ina taredaku ,cikin masu saura-ron halakarku. (Akayi musu azabada kansakali ranar Ba-dar).

أَمْ تَأْمُرُهُمْ أَحْلَٰمُهُم بِهَٰذَا أَمْ هُمْ قَوْمٌ طَاغُونَ ﴿30﴾
أَمْ يَقُولُونَ تَقَوَّلَهُۥ بَل لَّا يُؤْمِنُونَ ﴿31﴾ فَلْيَأْتُوا بِحَدِيثٍ مِّثْلِهِۦ
إِن كَانُوا صَٰدِقِينَ ﴿32﴾ أَمْ خُلِقُوا مِنْ غَيْرِ شَيْءٍ أَمْ هُمُ الْخَٰلِقُونَ ﴿33﴾
أَمْ خَلَقُوا السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضَ بَل لَّا يُوقِنُونَ ﴿34﴾ أَمْ عِندَهُمْ خَزَآئِنُ
رَبِّكَ أَمْ هُمُ الْمُصَيْطِرُونَ ﴿35﴾ أَمْ لَهُمْ سُلَّمٌ يَسْتَمِعُونَ فِيهِ
فَلْيَأْتِ مُسْتَمِعُهُم بِسُلْطَٰنٍ مُّبِينٍ ﴿36﴾ أَمْ لَهُ الْبَنَٰتُ وَلَكُمُ الْبَنُونَ ﴿37﴾
أَمْ تَسْئَلُهُمْ أَجْرًا فَهُم مِّن مَّغْرَمٍ مُّثْقَلُونَ ﴿38﴾ أَمْ عِندَهُمُ
الْغَيْبُ فَهُمْ يَكْتُبُونَ ﴿39﴾ أَمْ يُرِيدُونَ كَيْدًا فَالَّذِينَ كَفَرُوا
هُمُ الْمَكِيدُونَ ﴿40﴾ أَمْ لَهُمْ إِلَٰهٌ غَيْرُ اللَّهِ سُبْحَٰنَ اللَّهِ
عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿41﴾ * وَإِن يَرَوْا كِسْفًا مِّنَ السَّمَآءِ سَاقِطًا ثمن
يَقُولُوا سَحَابٌ مَّرْكُومٌ ﴿42﴾ فَذَرْهُمْ حَتَّىٰ يَلْقَوْا يَوْمَهُمُ الَّذِي
فِيهِ يُصْعَقُونَ ﴿43﴾ يَوْمَ لَا يُغْنِي عَنْهُمْ كَيْدُهُمْ شَيْئًا وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ ﴿44﴾
وَإِنَّ لِلَّذِينَ ظَلَمُوا عَذَابًا دُونَ ذَٰلِكَ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿45﴾
وَاصْبِرْ لِحُكْمِ رَبِّكَ فَإِنَّكَ بِأَعْيُنِنَا وَسَبِّحْ بِحَمْدِ رَبِّكَ
حِينَ تَقُومُ ﴿46﴾ وَمِنَ الَّيْلِ فَسَبِّحْهُ وَإِدْبَٰرَ النُّجُومِ ﴿47﴾

30. Shin hankulan sune suke umar-ninsu da wannan magana, (faɗinsu gareshi boka ne, mawald ne da sauransu, a'a hankula bazasu umarce su da wannan ba), bari! Sudai mutane ne masu shishshigi.
31. Bari! suna cewa: "Y kirkiri Alƙur'ani ne, a'a bai kirkire shi ba, Sudai basu bada gaskiya bane (don girman kai, to in sunce ƙirƙirarsa yayi).
32. To su zo dan zance abin kirkira kamarsa in sun kasance magas-gata (a cikin faɗinsu).
33. Ko an haliccesune bada maha-licci ba (a'a) ko ko sune suka halicci kawukansu, (a'a) ba a hankaltar abin halitta bada ma-licci ba, wala rashashshe dazaiyi halitta, ba makawa daga gare-su cewa mahaliccinsu Shine Allah, to saboda me bazasu kadaitashi su bada gaskiya da manzonsa da littafinsa ba?).
34. Ko sun halicci sammai da ƙassai ne? (La! a'a, ba mai iko bisa halittarsu sai Allah mahalicci, to saboda me basa bauta masa?) Bari! su basu sakankance dashi ba, (indasun sakankance dashi, dasun bada gaskiya da Anna-binsa).
35. Ko taskokin Ubangijinka suna gurinsune (na Annabci da arzi-ki da waninsu, su kebanci wanda suka ga dama da abinda suka ga dama? a'a), koko sune masu jabberanci (a kan abubu-wa, su aikata abinda suka ga dama yanda suka ga dama, a'a).
36. Ko suna da tsanine (izuwa sama, sujiyo jayaiya da Annabi Sallallahu alaihi wa sallama a kan riyawarsu? to in sun yi da awar haka), to mai sauraron jin nasu yazo musu da hujja ma-baiyaniya (saboda irin wannan riyawa tayi kama da cewarsu mala'iku 'ya'yan Allah ne, sai Allah Ta'ala yace).
37. Ko yana da 'ya'ya mata (a riy-awarku?) Kuna da mazaje? (Ubangiji ya girma ga buran wannan riyawa).
38. Ko ka tambaye su lada ne a kan abinda ka zo musu dashi na (addini), to suka zama ababan nauyayawa, (daga biyan wan-nan ladan)?
39. Ko suna sanin gaibu ne, su suna rubuta (gaibun har su sami da-mar jayaiya da Annabi Sallalla-hu alaihi wa sallama, a cikin ta-shin alƙiyama da al'amaran lahira da riyawarsu?).
40. Ko suna nafin kaidi dakai ne, (domin su halakad dakai a gi-dan shawara, wanda ake ce dashi Darin Nadawati)? to waɗanda suka kafirta sune aba-ban halakarwa, (to sai Allah ya kiyaye shi daga sharrinsu ya halakad dasu a ranar Badar).
41. Ko suna da wani Ubangiji ba Allah ba? Tsarki ya tabbata ga Allah gaburan abinda suke shir-kantashi (dashi na daga iyayen giji, istifhamin nan na am a waɗannan gurare, don nunawa ne da umstawa garesu.)
42. Idan sun ga wani yanki na daga sama ya saryo (a kansu tamfar da sukace "a saryo dayanki na daga sama a kansu", don azab-tarwa garesu), saisu ce: "Wan-nan girgije ne mai hauhawan juna, (zamu Koshi da ruwansa, bazasu bada gaskiya ba).
43. To rabu dasu har su gamu da ra-narsu wacce suke mutuwa a cikinsa, (wato Shine Badar).
44. Ranar da kaidinsu bazai wadatar dasu komai ba, su baza a hana masu azabar Lahira ba.
45 Haƙiƙa waɗanda suka zalinci kansu (da kafirci) suna da azabakuma bayan wancanenka (a du-niyagaban mutuwarsu, an yi musu azabada yunwa shekara bakwai kuma da kisa a ranar Badar), saidai yawaicinsu, basu san (cewa azabazata sauka garesu ba).

(CIKA SURA DA UMARNI DA HAƘURI DA KULAWA DA SALLOLI BIYAR DA AURADU BAYAN SALLOLI)

46. Sai kayi hakuri da hukuncin Ubangrjinka (da jinkirin dayayi musu, kada kirjinka yakuntata), haƙiƙa kai, kana a maganar-mu, (muna kiyayeka, muna kula da kai, muna dubanka), kayi tasbihi ka hada da godiyar Ubangijinka, (kace SUBHA-NALLAHI WA BI HAMDIHI) lok-acin daka tashi (daga baccinka, ko daga mazauni).
47. Kuma da daddare kayi Tasbihi gareshi haƙiƙa tan da juyawar bayan taurari, (wato faduwarta ko ka sallaci Isha biyu a cikin na farko Shine MINALLAILI FA-SABBIHUHU, ana biyu ka sallaci Raka'atanul Fajri, ko kuma fa-rillar asuba wato Shine WA'IDABARAN NUJUMI).

سُورَةُ النَّجْمِ مَكِّيَّة 53

وَهِيَ إِحْدَىٰ وَسِتُّونَ ءَايَة 61

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

وَالنَّجْمِ إِذَا هَوَىٰ ﴿1﴾ مَا ضَلَّ صَاحِبُكُمْ وَمَا غَوَىٰ ﴿2﴾ وَمَا يَنطِقُ عَنِ الْهَوَىٰ ﴿3﴾
إِنْ هُوَ إِلَّا وَحْيٌ يُوحَىٰ ﴿4﴾ عَلَّمَهُ شَدِيدُ الْقُوَىٰ ﴿5﴾ ذُو مِرَّةٍ فَاسْتَوَىٰ ﴿6﴾
وَهُوَ بِالْأُفُقِ الْأَعْلَىٰ ﴿7﴾ ثُمَّ دَنَا فَتَدَلَّىٰ ﴿8﴾ فَكَانَ قَابَ قَوْسَيْنِ أَوْ أَدْنَىٰ ﴿9﴾
فَأَوْحَىٰ إِلَىٰ عَبْدِهِ مَا أَوْحَىٰ ﴿10﴾ مَا كَذَبَ الْفُؤَادُ مَا رَأَىٰ ﴿11﴾ أَفَتُمَارُونَهُ عَلَىٰ
مَا يَرَىٰ ﴿12﴾ وَلَقَدْ رَءَاهُ نَزْلَةً أُخْرَىٰ ﴿13﴾ عِندَ سِدْرَةِ الْمُنتَهَىٰ ﴿14﴾ عِندَهَا جَنَّةُ
الْمَأْوَىٰ ﴿15﴾ إِذْ يَغْشَى السِّدْرَةَ مَا يَغْشَىٰ ﴿16﴾ مَا زَاغَ الْبَصَرُ وَمَا طَغَىٰ ﴿17﴾ لَقَدْ
رَأَىٰ مِنْ ءَايَاتِ رَبِّهِ الْكُبْرَىٰ ﴿18﴾ أَفَرَأَيْتُمُ اللَّاتَ وَالْعُزَّىٰ ﴿19﴾ وَمَنَوٰةَ الثَّالِثَةَ
الْأُخْرَىٰ ﴿20﴾ أَلَكُمُ الذَّكَرُ وَلَهُ الْأُنثَىٰ ﴿21﴾ تِلْكَ إِذًا قِسْمَةٌ ضِيزَىٰ ﴿22﴾
إِنْ هِيَ إِلَّا أَسْمَاءٌ سَمَّيْتُمُوهَا أَنتُمْ وَءَابَاؤُكُم مَّا أَنزَلَ اللَّهُ بِهَا مِن سُلْطَانٍ
إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا الظَّنَّ وَمَا تَهْوَى الْأَنفُسُ وَلَقَدْ جَاءَهُم مِّن رَّبِّهِمُ الْهُدَىٰ ﴿23﴾
أَمْ لِلْإِنسَانِ مَا تَمَنَّىٰ ﴿24﴾ فَلِلَّهِ الْآخِرَةُ وَالْأُولَىٰ ﴿25﴾ * وَكَم مِّن مَّلَكٍ فِي السَّمَاوَاتِ
لَا تُغْنِي شَفَاعَتُهُمْ شَيْئًا إِلَّا مِن بَعْدِ أَن يَأْذَنَ اللَّهُ لِمَن يَشَاءُ وَيَرْضَىٰ ﴿26﴾

ربع

Wannan sura Itace Suratu Najami

a Makka aka saukar da ita. Aya sittin da ɗayace (61)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinfan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe

(Wannan sura ta tabbatar da Risala da Gaskiyar Manzon Allah Sallallahu alaihi wa sallama ccwa Alƙur'ani daga Allah yake da zance kan Gumaka sunannaki ne da ababan anbato gareta, da zance kan Zatin Allah Subaha-nahu Wa Ta'ala da bayanin ayoyinsa a cikin halittada wasu ha££oki na musulunci da aka samesu a cikin ba'alin littattafai).

(TABBATAR DA AL'AMARIN WAHAYI)

1. Ubangiji ya rantsc da tauraron Suraiya lokacin daya faɗi.
2. Abokinku (Annabi Sallallahu alaihi wa sallama), bai ɓace ga buran hanyar shiriya ba, da ai-kata saɓo, bai taɓa faɗawa cikin jahilci na wani abu ba, (bai taɓa aikin wauta na jahiliyya ba). **3.** Baya furuci a kan son zuciya. **4.** Shi bai kasance basai wahayi da ake aikowa izuwa gareshi. **5.** Mai tsananin karfafe-karfafe na zahiri, Shine ya aiko shi (Shine Mala'ika Jibrilu.)
6. Ma'abocin karfi na badini sai yayi daidai.
7. Alhali yana cikin sassa mafi ɗaukaka, (wato sassan rana yay-in hudowarta, a bisa surarsa wacce Allah ya halicce shi a kanta, Manzon Allah yagan shi, alhali yana cikin kogon Hira, ya toshe sassa har izuwa faɗin *rana, ya facG yana sumamme, ya* kasance ya tambaye shiya nuna masa kansa a kan suratasa wacce Allah ya halicce shi a kanta, yayi masa alkawari zai baiyana gareshi da haka din a kogon Hira. To sai Jibrilu ya sauko masa a surarsa ta 'yan Adam. **8.** Sannan yakusanta daga gareshi, ya ƙara kusanci. **9.** Ya zama daga gareshi gwargwa-don bakabiyu ko mafi kusanci daga wannan, (har ya farka zu-ciyarsa ta nutsu).
10. Ubangiji ya aiko izuwa bawansa (Annabi Muhammadu Sallalla-hu alaihi wa sallama) abinda ya aiko, (ba a faɗi abinda ya aiko dashi ba, saboda girman sha'aninsa. Malam yace: "Na fassara ayar a bisa abinda Shchu Mahalli ya fassara ta nc wato shiya fassara ABDIHI da Jibrila, Malan kuma ya fassara shi da Manzon Allah saboda a cewar Malan Tafsiri da Hadisi-Sawi").
11. Zuciyar Annabi (Sallallahu alai-hi wa saliama) bata ƙaryata abinda yaganiba. **12.** Shin kwadinga jayaiya dashi a cikin abinda yake gani (na zatin Ubangiji.) 13. Haƙiƙa yaga Ubangiji marratan. **14.** Nan ga magaryar tukewa, (zam-anin dayayi tafiyar dare dashi, magaryace a dama da aParshi, ba wanda yake ketare ta na An-nabi ko Mala ika).
15. Jannatul ina'awa tana nan gareta (Mala'iku suna komawa izuwa garetada rayukan Shahidai da masu tsoron Allah). **16.** Zamanin da abinda yake lullube magarya yake lullubeta (na daga tsuntsu da haske da waninsu na daga abinda ban da Allah ba wanda yasan shi).
17. Ganin (Manzon Allah bai kar-kace ba, kuma bai ketare (abin ganinsa ba, a wancanenka dare).
18. Haƙiƙa yaga daga ayoyin Ubangijinsa maigira (a cikin wannan dare yaga ba'alinta, daga aja'ibil malakuti, yaga gadon lilo kore, wanda ya toshe sassan sama, yaga Jibrilu yana da fif-fike dari shida kuma yaga Ubangiji Subhanahu wa Ta'ala) kamar yadda Siyudl ya tabbatar a Suratul Isra'i da Hadisi wanda Hakimu ya ruwaito shi a cikin Mustadraku).

(WANNAN SUNE IYAYEN GIJINSU WAƊANDA BAZASU WADATAD DASU KOMAI BA)

19. Shin, ku bani labari Latada Uzza. **20.** Da manata ta ukun din biyun (da suka gabata wulafcantacciya, ita gumakace ta dowarwatsu, mu-shurikai suka bauta mata suna riyawar cewa za tayi ceto gare-su nan ga Allah, ma'ana ku bani labari shin waɗannan gumaka suna da ikone bisa wani abu komai ƙanƙantarsa kuke bauta mata ba Allah ba mai iko bisa abinda anbatonsa yagabata? A yayin da suka riyacewa Mala'iku 'ya'yan Allah ne, tare ^ da (an 'ya'ya mata dasuke yi sai Allah ya saukar da). **21.** Shin mazaje ne naku? Shi kuma Ubangiji mataye ne nasa? **22.** Wancanenka rabo ce ta cin zali.

(KUSKUREN WAHABIYA DATA ɗAUKI ANNABAWA DA WALIYAI A MATSAYIN GUMAKA NAN GA MASOYANSU).

23. Ita waɗannan abubuwa bata ka-sance ba, sai sunannaki da kukayi anabato da ita, kuda iyayen-ku, (kuka anbace ta gumaka kuke bauta mata) Allah bai sau-kad da hujja a kan bautarta =

إِنَّ ٱلَّذِينَ لَا يُومِنُونَ بِالْاخِرَةِ لَيُسَمُّونَ ٱلْمَلَٰٓئِكَةَ تَسْمِيَةَ ٱلْأُنثَىٰ ﴿27﴾
وَمَا لَهُم بِهِۦ مِنْ عِلْمٍ إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّ وَإِنَّ ٱلظَّنَّ لَا يُغْنِي مِنَ
ٱلْحَقِّ شَيْـًٔا فَأَعْرِضْ عَن مَّن تَوَلَّىٰ عَن ذِكْرِنَا وَلَمْ يُرِدْ
إِلَّا ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَا ﴿28﴾ ذَٰلِكَ مَبْلَغُهُم مِّنَ ٱلْعِلْمِ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعْلَمُ
بِمَن ضَلَّ عَن سَبِيلِهِۦ وَهُوَ أَعْلَمُ بِمَنِ ٱهْتَدَىٰ ﴿29﴾ وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَمَا فِي ٱلْأَرْضِ لِيَجْزِيَ ٱلَّذِينَ أَسَٰٓـُٔواْ بِمَا عَمِلُواْ
وَيَجْزِيَ ٱلَّذِينَ أَحْسَنُواْ بِٱلْحُسْنَى ﴿30﴾ ٱلَّذِينَ يَجْتَنِبُونَ
كَبَٰٓئِرَ ٱلْإِثْمِ وَٱلْفَوَٰحِشَ إِلَّا ٱللَّمَمَ إِنَّ رَبَّكَ وَٰسِعُ ٱلْمَغْفِرَةِ
هُوَ أَعْلَمُ بِكُمُۥٓ إِذْ أَنشَأَكُم مِّنَ ٱلْأَرْضِ وَإِذْ أَنتُمُۥٓ أَجِنَّةٞ فِي بُطُونِ
أُمَّهَٰتِكُمْ فَلَا تُزَكُّوٓاْ أَنفُسَكُمْ هُوَ أَعْلَمُ بِمَنِ ٱتَّقَىٰ ﴿31﴾ أَفَرَآيْتَ
ٱلَّذِي تَوَلَّىٰ ﴿32﴾ وَأَعْطَىٰ قَلِيلًا وَأَكْدَىٰ ﴿33﴾ أَعِندَهُۥ عِلْمُ ٱلْغَيْبِ فَهُوَ يَرَىٰ ﴿34﴾
أَمْ لَمْ يُنَبَّأْ بِمَا فِي صُحُفِ مُوسَىٰ ﴿35﴾ وَإِبْرَٰهِيمَ ٱلَّذِي وَفَّىٰ ﴿36﴾
أَلَّا تَزِرُ وَازِرَةٞ وِزْرَ أُخْرَىٰ ﴿37﴾ وَأَن لَّيْسَ لِلْإِنسَٰنِ إِلَّا مَا سَعَىٰ ﴿38﴾
وَأَنَّ سَعْيَهُۥ سَوْفَ يُرَىٰ ﴿39﴾ ثُمَّ يُجْزَىٰهُ ٱلْجَزَآءَ ٱلْأَوْفَىٰ ﴿40﴾ وَأَنَّ إِلَىٰ رَبِّكَ
ٱلْمُنتَهَىٰ ﴿41﴾ وَأَنَّهُۥ هُوَ أَضْحَكَ وَأَبْكَىٰ ﴿42﴾ وَأَنَّهُۥ هُوَ أَمَاتَ وَأَحْيَا ﴿43﴾

= ba, ba kwa bin komai a cikin bau-tarta sai zato da abinda zu-ciyoyi suke so, (wato abinda shaiɗan ya ƙawata masu, cewa ita tana ceto garesu nan ga Allah), haƙiƙa shiriya tazo musu daga Ubangijinsu (da hujja yan-kakkiya, basu komo ga buran abinda suke kai ba.

24. Shin kowane mutum daga cikin-su yana da abinda ya gurta?(Shine cewa gumaka tana ceto garesu, a'a). **25.** Duniya da lahira na Allah ne (ba abindazai afku a cikinsu sai abinda Allah ya nufa). **26.** Da yawa Mala'iku a sama a cikin sammai (tareda girman da Allah ya basu), cetonsu bazata anfana masu komai ba, sai bay-an Allah yayi izini garesu a cikinsa ga wanda yaga dama daga bayinsa ya yarda dashi, (saboda fadinsa basa yin ceto sai ga wanda Allah ya yarda da cetonsa, an sani cewa ceto ba a sammunsa sai bayan izini daga gareshi saboda Ubangiji yace: ba mai ceto gurin Allah saida izininsa.)

27. WacTanda basu bada gaskiya da Lahira ba lallai suna anbaton Mala'iku mata, (suna cewa AL MALA'IKATU BANATULLAHI.)

28. Basu da wani sani da wannan zance, basa bin komai cikinsa sai zato, shi zato baya wadatar da komai na daga gaskiya (wato ilimi, wato abinda ake neman ilimi cikinsa, baya buRatar ko-mai na zato, sai al'amura na Kudure-Kudure na tauhidi, ban da Amaliyatu, wato aikace-aikace bakudure-Rudure ba, sa-boda Ayimmatu sun sassaba a cikin rassoshi na fildhu, wato sanin Allah da manzanni da abinda sukazo dashi labudda a sami ilimi a cikinsa wato yanke-wa mai da cewa da gaskiya ta-kan dalili, amma rassan addini to rinjayen zato yana wadatarwa a cikinta - Sawi), rabu da wanda ya juya bayaga buran anbaton-mu, bai nufi komai basai rayu-war duniya.

29. Wancananka (neman duniya) Shine matukar saninsu (Don sun , fi-fita duniya a kan lahira,) Ubangijinka Shine masani da wanda ya shiriya.

30. Abinda yake sammai da ƙassaina Allah ne, (yana shiryar da wanda yaga dama yana ɓatar da · wanda yaga dama) donya sa-kawa waɗanda sukayi mummu-nan aiki na shirka da abinda suka aikata ya sakawa waɗanda sukayi kyakkyawan aiki (na da'a da tauhidi) da Aljanna.

(SU WAYE MASU KYAKKYAWAN AIKI)

31. Sune waɗanda suke nisantar manya-manyan zunubbai, da aiyukan alfasha sai fcanKananan zunubbai (kamar dubadasum-ba, da shafa, wannan Allah yana gafartasu saboda nisantar man-ya-martyan zunub^ai - manya-manyan zunubbai sune abinda narko yazo a cikinta ko haddi. Fashisha kuma Itace abinda bama mai girma take cikinta, kamar zina da satada kisan kai da sauransu), Ubangijinka may-alwacin gafara ne ga wancanan-ka da karbar tuba, wannan aya ta sauka cikin wanda yake cewa "Sallarnu, Azuminmu, Hajjin-mu") Allah ne masani daku ,zamanin daya fareku daga cikin I lasa, (da halittar ubanku Anna-bi Adamu daga turbaya) da kuma sanda kuke tayiyyuka a cikin cikkunan mahaifanku, to kadaku ,tsarkake kanku (wato kadaku ,yabeta a bisa hanyar ji ji dakai amma a bisa hanyar fu-rici da ni'imar Ubangiji kyak-kyawa ne, irin sune maganga-nun da W'aliyai sukayi wanda ake kira Tahaddusi da ni'imar Ubangiji) Shine masani da wanda yake jin tsoron Allah.

(HAIcKOKI NA MUSULUNCI)

32. Bamu labarin wanda ya bada bayaga buran imani (wato yayi riddayayin da akayi masa gori na musulunci yace shi yana jin tsoron azabar Allah, wanda yayi masa gorin yace ya laminće masa azabar Allah, in yakoma izuwa mushurukancinsa, ya bashi wani daga dukiyarsa yakoma ga buran musuluncin).

33. Ya bada kaɗan (daga dukiyar daya ambata) ya dakushe ga ra-gowar, (wato ya hana).

34. Shin yana da sanin gaibu a gu-rinsa ne (wato shi yana ganin galbu? a'a, Shine Walidu dan Mugira). **35.** Bari! ba a bashi labari da abinda kc cikin littattafan Annabi Musa ba. **36.** Da Annabi Ibrahim wanda ya cika (abinda aka umarce dashi). **37.** Wata kai bazata dauki zunubin wata kai ba. **38.** Cewa mutum (wato kafiri) bashi da komai sai abinda ya ai-kata. **39.** Haƙiƙa aikinsa da sannu za a gan shi (a Lahira). **40.** Sannan a saka masa sakamako mafi cika.

41. Haƙiƙa matukar tulcewa ta tabbata izuwa Ubangijinka, (bayan mutuwa zaiyi musu sakamako).

42. Haƙiƙa shi Ubangiji ne Shine ya darekad da wanda yaga dama, (wato ya faranta masa,) yakokadda wanda yaga dama (wato ya baƙanta masa.)

43. Kuma shiya matar (a duniya) ya raya (saboda tashi).

وَأَنَّهُۥ خَلَقَ ٱلزَّوْجَيْنِ ٱلذَّكَرَ وَٱلْأُنثَىٰ ﴿٤٥﴾ مِن نُّطْفَةٍ إِذَا تُمْنَىٰ ﴿٤٦﴾
وَأَنَّ عَلَيْهِ ٱلنَّشْأَةَ ٱلْأُخْرَىٰ ﴿٤٧﴾ وَأَنَّهُۥ هُوَ أَغْنَىٰ وَأَقْنَىٰ ﴿٤٨﴾ وَأَنَّهُۥ هُوَ
رَبُّ ٱلشِّعْرَىٰ ﴿٤٩﴾ وَأَنَّهُۥ أَهْلَكَ عَادًا ٱلْأُولَىٰ ﴿٥٠﴾ وَثَمُودَا فَمَا أَبْقَىٰ ﴿٥١﴾
وَقَوْمَ نُوحٍ مِّن قَبْلُ إِنَّهُمْ كَانُوا هُمْ أَظْلَمَ وَأَطْغَىٰ ﴿٥٢﴾ وَٱلْمُؤْتَفِكَةَ
أَهْوَىٰ ﴿٥٣﴾ فَغَشَّىٰهَا مَا غَشَّىٰ ﴿٥٤﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكَ تَتَمَارَىٰ ﴿٥٥﴾
* هَٰذَا نَذِيرٌ مِّنَ ٱلنُّذُرِ ٱلْأُولَىٰٓ ﴿٥٦﴾ أَزِفَتِ ٱلْآزِفَةُ ﴿٥٧﴾ لَيْسَ لَهَا مِن دُونِ ٱللَّهِ ثمن
كَاشِفَةٌ ﴿٥٨﴾ أَفَمِنْ هَٰذَا ٱلْحَدِيثِ تَعْجَبُونَ ﴿٥٩﴾ وَتَضْحَكُونَ
وَلَا تَبْكُونَ ﴿٦٠﴾ وَأَنتُمْ سَٰمِدُونَ ﴿٦١﴾ فَٱسْجُدُوا لِلَّهِ وَٱعْبُدُوا ﴿٦٢﴾

54 سُورَةُ ٱلْقَمَرِ مَكِّيَّةٌ
وَهِيَ خَمْسٌ وَخَمْسُونَ ءَايَةً 55

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱقْتَرَبَتِ ٱلسَّاعَةُ وَٱنشَقَّ ٱلْقَمَرُ ﴿١﴾ وَإِن يَرَوْا ءَايَةً يُعْرِضُوا وَيَقُولُوا
سِحْرٌ مُّسْتَمِرٌّ ﴿٢﴾ وَكَذَّبُوا وَٱتَّبَعُوا أَهْوَآءَهُمْ وَكُلُّ أَمْرٍ مُّسْتَقِرٌّ ﴿٣﴾
وَلَقَدْ جَآءَهُم مِّنَ ٱلْأَنۢبَآءِ مَا فِيهِ مُزْدَجَرٌ ﴿٤﴾ حِكْمَةٌۢ بَٰلِغَةٌ
فَمَا تُغْنِ ٱلنُّذُرُ ﴿٥﴾ فَتَوَلَّ عَنْهُمْ يَوْمَ يَدْعُ ٱلدَّاعِ إِلَىٰ شَيْءٍ نُّكُرٍ ﴿٦﴾

44. Kuma lallai Shine ya halicci nau'i biyu namiji da mace.
45. Daga kwayar ruwan namiji;
zamanin da ake zubata a cikin mahaifa.
46. Kuma haƙiƙa tayarwa da tasar-wa suna ga Ubangiji (wato tana kansa saboda tashin alƙiyama bayan halittar farko.)
47. Kuma haƙiƙa Shine ya wadata (kowa da gwargwadon isuwa na dukiya) Shine ya bada dukiya da ake rike ta.
48. Haƙiƙa kuma Shine Ubangijin Shi'ira (tauraro ne bayan Jau-za'u ana bauta mata a cikin Jahiliyya).
49. Kuma haƙiƙa Shine ya halakar da Adu ta farko (mutanen Anna-bi Hudu da Adu ta biyu muta-nen Annabi Salihu).
50. Da Samudu (mutanen Annabi Salihu), baiwanzar da ko daya (daga cikinsu ba).
51. Ya halakar da mutanen Annabi Nuhu tun gaban (Adu da Samudu), haƙiƙa su sun kasance sune mafi zalinci, mafi shishshigi (daga Adu da Samudu saboda tsawon zaman Annabi Nuhu a cikinsu, ya zauna a cikinsu she-kara dubu sai shekara hamsin ne babu, sun kasance tareda rashin bada gaskiyarsu dashi, suna cutarsa suna ta dukansa).
52. Alkaryun mutanen Annabi Hudu sune mu'utafika (wato mai kawa daga inda take) ya kifar da ita, (bayan ya daga ta izuwa sama a juye izuwa kasa, daya umarci Jibrila dayin haka).
53. Saiya lullubetada abinda ya lullubeta (dashi na daga duwar-watsu yace an yi ibhamin abinda aka lullube ta dashi don ban tsoro a cikin Hudu muka sanya samanta kasanta muka sako da ruwa a kansu na konannen dut-sen jahannama.
54. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinka kake kokonto (ya kai mutum kafiri ko kake karya-tawa?).
55. Wannan (Annabi Sallallahu alai-hi wa sallama) mai gargadi ne daga masu gargaɗin farko.
56. alƙiyama ta kusa.
57. Ba mai yayewa gareta sai Allah, (wato ba mai baiyana sandaza ayi ta sai Allah).
58. Shin to daga wannan zance (Shine alƙur'ani) kuke yin mana ki na ƙaryatawa?
59. Kuke dariya (don izgili) ba kwa kuka (don gargaɗinsa da narkonsa?).
60. Alhali ku kuna marafkana (ga buran abinda ake nema daga gareku?).
61. To kuyi sajada ga Allah (wanda ya haliccceku). Kuyi bauta, kada kuyi sujjada ga gumaka, kadaku ,bauta mata).

Wannan sura Itace Suratu Kamari

A Makka aka saukar da ita. Aya hamsin da biyar ce (55)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinfan talikai a duniyagaba ɗaya, maijirJcan Muminai a Lahira a keɓe

(Wannan sura ta ƙunshi alkawari da narko da labaran al'ummar data wuce da wa'azantuwa da kuma ban tsoro ga kafirai da ambaton abinda yake samunsu ranar aliciyama, da abinda masu tsoron Allah suke samu na sakama-ko a cikin aljannar gaskiya).

1. AlƘiyama ta kusanta: wanta ya tsage (tsagi biyu a kan Abi Ku'aisin da Abi Ku'aiki'ana, ayace ga ma'aikin Allah SallAllahu alaihi wa sallama, alhali an roke shi ita, to sai yace: "Ku shaida da cewa ni ma'aikin Allah ne".
2. In kafiran Kuraishu suka ga aya (wato mu'ujizata manzon Allah Sallallahu alaihi wa sallam) saisu bijire su ce "Wannan tsafi ne mai karfi".
3. .Sun ƙaryata (manzon Allah Sal-lallahu alaihi wa sallama) sun bi soye-soyen zuciyarsu (a cikin aikin barna) dukkan lamari na khairi ko sharri) zai tabbata ne ga masu shi, (a cikin wuta ko a aljanna).
4. Haƙiƙa abinda tsautuwa yake cikinsa (na labarai) yazo musu.
5. Wannan hikima ce cikakkiya, Menene masu gargadi zasu an-fana?
6. Rabu dasu ranar da mai kira yayi kira (Shine Israfilu) dasuke fita bayan nan izuwa abu mum-muna (a cikin rai Shine hisabi).

خُشَّعًا أَبْصَٰرُهُمْ يَخْرُجُونَ مِنَ ٱلْأَجْدَاثِ كَأَنَّهُمْ جَرَادٌ مُّنتَشِرٌ ﴿٧﴾
مُّهْطِعِينَ إِلَى ٱلدَّاعِ يَقُولُ ٱلْكَٰفِرُونَ هَٰذَا يَوْمٌ عَسِرٌ ﴿٨﴾ كَذَّبَتْ
قَبْلَهُمْ قَوْمُ نُوحٍ فَكَذَّبُوا۟ عَبْدَنَا وَقَالُوا۟ مَجْنُونٌ وَٱزْدُجِرَ ﴿٩﴾
فَدَعَا رَبَّهُۥٓ أَنِّى مَغْلُوبٌ فَٱنتَصِرْ ﴿١٠﴾ فَفَتَحْنَآ أَبْوَٰبَ ٱلسَّمَآءِ بِمَآءٍ
مُّنْهَمِرٍ ﴿١١﴾ وَفَجَّرْنَا ٱلْأَرْضَ عُيُونًا فَٱلْتَقَى ٱلْمَآءُ عَلَىٰٓ أَمْرٍ قَدْ قُدِرَ ﴿١٢﴾
وَحَمَلْنَٰهُ عَلَىٰ ذَاتِ أَلْوَٰحٍ وَدُسُرٍ ﴿١٣﴾ تَجْرِى بِأَعْيُنِنَا جَزَآءً
لِّمَن كَانَ كُفِرَ ﴿١٤﴾ وَلَقَد تَّرَكْنَٰهَآ ءَايَةً فَهَلْ مِن مُّدَّكِرٍ ﴿١٥﴾
فَكَيْفَ كَانَ عَذَابِى وَنُذُرِ ﴿١٦﴾ وَلَقَدْ يَسَّرْنَا ٱلْقُرْءَانَ لِلذِّكْرِ فَهَلْ مِن
مُّدَّكِرٍ ﴿١٧﴾ ۞ كَذَّبَتْ عَادٌ فَكَيْفَ كَانَ عَذَابِى وَنُذُرِ ﴿١٨﴾ إِنَّآ أَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ ربع
رِيحًا صَرْصَرًا فِى يَوْمِ نَحْسٍ مُّسْتَمِرٍّ ﴿١٩﴾ تَنزِعُ ٱلنَّاسَ كَأَنَّهُمْ أَعْجَازُ نَخْلٍ مُّنقَعِرٍ ﴿٢٠﴾
فَكَيْفَ كَانَ عَذَابِى وَنُذُرِ ﴿٢١﴾ وَلَقَدْ يَسَّرْنَا ٱلْقُرْءَانَ لِلذِّكْرِ فَهَلْ مِن مُّدَّكِرٍ ﴿٢٢﴾
كَذَّبَتْ ثَمُودُ بِٱلنُّذُرِ ﴿٢٣﴾ فَقَالُوٓا۟ أَبَشَرًا مِّنَّا وَٰحِدًا نَّتَّبِعُهُۥٓ إِنَّآ إِذًا
لَّفِى ضَلَٰلٍ وَسُعُرٍ ﴿٢٤﴾ أَءُلْقِىَ ٱلذِّكْرُ عَلَيْهِ مِنۢ بَيْنِنَا بَلْ هُوَ كَذَّابٌ
أَشِرٌ ﴿٢٥﴾ سَيَعْلَمُونَ غَدًا مَّنِ ٱلْكَذَّابُ ٱلْأَشِرُ ﴿٢٦﴾
إِنَّا مُرْسِلُوا۟ ٱلنَّاقَةِ فِتْنَةً لَّهُمْ فَٱرْتَقِبْهُمْ وَٱصْطَبِرْ ﴿٢٧﴾

7. Sannan su suna wulakantattu, suna fita daga cikin kaburbura kai kace fari ne madaidaita.
8. Masu gaggawa suna mika wuy-aye izuwa makirayi. Kafirai daga cikinsu suna cewa: "Wan-nan rana ce mawuyaciya bisa kafirai").

(AkIBAR MASU KARYATAWA DAGA ADU DA SAMUDU DA ALI-FIR'AUNA)

9. Mutanen Annabi Nuhu (alaihis-salamu) sun karyata (Annabi Nuhu alaihissalamu) gaban kuraishawa, suka karyata baw-anmu Annabi Nuhu sukace:"Tababbe ne, sukayi masa tsawa da zagi da waninsa.
10. Saiya rofa Ubangijinsa " Hakika ni abin rinjaye ne, ka ki mini dauki dayi musu azaba".
11. Sai muka kece kofofin sama da ruwa mai tsugewa tsuga mai tsanani.
12. Muka keto idanuwan kasa m-wan sama dana kasa suka gamu a kan al'amari da aka kaddara shi tun azal, (Shine halakar dasu da nutsewa).
13. Muka dauki Annabi Nuhu a kan jirgi ma'abociyar alluma da kusoshi.
14 Tana gudu amagana daga garemu abar kiyayewa (an nutsar dasune da azaba) don sakamako ga wanda aka kafirce dashi (Shine Annabi Nuhu alaihissalamu).
15. Hakika mun wanzar da wannan aiki don aya (wato izna ga wan-dazaiyi izna da ita) shin akwai mai wa'azantuwa (da ita?).
16. To yaya azabata ta kasance da gargadi na? (ta afku gurin afRuwarta ya Ubangiji!).
17. Hakika mun horc alkur'ani don haddacewa, akwai mai wa'azantuwa ya haddacc shi? da ka, daga littafian ake hadda-cewa da ka, daga littafin Allah ababan saukarwa sai Alkur'ani). (KISSAR ADU)
18. Adawa sun karyata (Annabinsu Annabi Hudu, akayi musu aza-ba), yaya azabata ta kasance, da gargadina (garesu da azaba, ka-fin saukar azabar? Ubangiji yayi bayanintada fadinsa...)
19. Hakika mun sako iska mai tsananin kara a kansu a cikin rana mai Nashisa shu'uma mai Karfin shu'umi madauwaminsa, (ya afku ranar Laraba a karshen wata).
20. Tana tunbuke mutane (daga ramukan kasa, wacTanda K:asa ta lullube su tana bugar dasu a kan kawukansu wuyayinsu ta karrarraye, gangar jiki daban, kai daban) kai kace su (alhali suna cikin wannan hali) tu-shiyoyi ne na dabino yankakke saryayye a kan kasa.
21. Yaya azabata ta kasance da gar-gadina (sun afku gurin afkuwar-su ya Ubangiji).
22. Hakika mun hore alkur'ani sa-boda haddacewa, to akwai mai wa'azantuwa?

(KISSAR SAMUDAWA)

23. Samudawa sun karyatada masu gargadi, (wato Annabi Salihu).
24. Sai sukace "Yaya zamu bi mu-tum guda daya daga cikinmu ba-wani sarki ba wato bazamu bi shi ba). Hakika mu in mun bi shi muna cikin batada hauka.
25. Yaya za a aiko masa da wahayi a tsakaiiinmu (wai ba a aiko izu-wa gaieshi ba), bari! shi maj^aryaci nc mai girman kai".
26. Ubangiji yace "da sannu zasu sani a ranar Lahira, waye makaryacin mai girman kai (Shine ko su, wato ayi musu azaba a bisa karyata Annabinsu Sali-hu. Ubangiji ya baiyanata).
27. Hakika mu masu fito da taguwa ne (daga fa tamfar da suka nema) don jarrabawa garesu sai ka saurare su (Ya Annabi Sali-hu, ka saurari abinda zasu ai-katada abindaza a aikata dasu!) Ka daure (bisa cutarsu).

وَنَبِّئْهُمُۥٓ أَنَّ ٱلْمَآءَ قِسْمَةُۢ بَيْنَهُمْۖ كُلُّ شِرْبٖ مُّحْتَضَرٞ ﴿28﴾ فَنَادَوْاْ
صَاحِبَهُمْ فَتَعَاطَىٰ فَعَقَرَ ﴿29﴾ فَكَيْفَ كَانَ عَذَابِے وَنُذُرِ ﴿30﴾
إِنَّآ أَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ صَيْحَةٗ وَاحِدَةٗ فَكَانُواْ كَهَشِيمِ ٱلْمُحْتَظِرِ ﴿31﴾
وَلَقَدْ يَسَّرْنَا ٱلْقُرْءَانَ لِلذِّكْرِ فَهَلْ مِن مُّدَّكِرٖ ﴿32﴾ كَذَّبَتْ قَوْمُ لُوطٍۢ بِالنُّذُرِ ﴿33﴾
إِنَّآ أَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ حَاصِباً اِلَّآ ءَالَ لُوطٖ نَّجَّيْنَٰهُم بِسَحَرٖ ﴿34﴾ نِّعْمَةٗ مِّنْ
عِندِنَا كَذَٰلِكَ نَجْزِے مَن شَكَرَ ﴿35﴾ وَلَقَدْ أَنذَرَهُم بَطْشَتَنَا فَتَمَارَوْاْ
بِالنُّذُرِ ﴿36﴾ وَلَقَدْ رَٰوَدُوهُ عَن ضَيْفِهِۦ فَطَمَسْنَا أَعْيُنَهُمْ فَذُوقُواْ عَذَابِے
وَنُذُرِ ﴿37﴾ وَلَقَدْ صَبَّحَهُم بُكْرَةً عَذَابٞ مُّسْتَقِرّٞ ﴿38﴾ فَذُوقُواْ عَذَابِے وَنُذُرِ ﴿39﴾
وَلَقَدْ يَسَّرْنَا ٱلْقُرْءَانَ لِلذِّكْرِ فَهَلْ مِن مُّدَّكِرٖ ﴿40﴾ * وَلَقَدْ جَآءَ ءَالَ فِرْعَوْنَ ثمن
ٱلنُّذُرُ ﴿41﴾ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا كُلِّهَا فَأَخَذْنَٰهُمْ أَخْذَ عَزِيزٖ مُّقْتَدِرٍ ﴿42﴾
أَكُفَّارُكُمْ خَيْرٞ مِّنْ اُوْلَٰٓئِكُمْ أَمْ لَكُم بَرَآءَةٞ فِے ٱلزُّبُرِ ﴿43﴾ أَمْ يَقُولُونَ
نَحْنُ جَمِيعٞ مُّنتَصِرٞ ﴿44﴾ سَيُهْزَمُ ٱلْجَمْعُ وَيُوَلُّونَ ٱلدُّبُرَ ﴿45﴾
بَلِ ٱلسَّاعَةُ مَوْعِدُهُمْ وَالسَّاعَةُ أَدْهَىٰ وَأَمَرُّ ﴿46﴾ إِنَّ ٱلْمُجْرِمِينَ
فِے ضَلَٰلٖ وَسُعُرٖ ﴿47﴾ يَوْمَ يُسْحَبُونَ فِے ٱلنَّارِ عَلَىٰ وُجُوهِهِمْ
ذُوقُواْ مَسَّ سَقَرَ ﴿48﴾ إِنَّا كُلَّ شَےْءٍ خَلَقْنَٰهُ بِقَدَرٖ ﴿49﴾

28. Ka basu labari cewa wancanen-ka ruwa abin rabawa ne tsaka-ninsu da tsakanin taguwa (wuni ɗaya nasu wani ɗaya nata) kow-ane nasibin ruwa, za a halaite shi (wato mutane su halarci ra-narsu, Taguwa ranarta, suka zarce a kan wannan. Sai sukayi nufi da kashe taguwar.
29. Sai suka kirawo abokinsu kudaru (domin ya kashe ta), ya kama kansakali ya sare ta (dashi don daccwa dasu).
30. Yaya azabata ta kasance garesu da gargaɗina (tun gaban sau-kowarsa? ya afku wajen afku-warsa, ya bayyana azabar da faɗinsa).
31. Haƙiƙa mun sakar musu tsawa a kansu guda ɗaya, suka zama kamar dandaka££en ganyayyaki na mai yin shinge (wanda yake yiwa tumakan&a shinge daga ƙeƙashashshen Itace da ƙaya, yana kikayanta daga namun daji dashi wannan shinge abinda ya sakai daga wancanenka aka tat-take shi Shine Hashimu).
32. HaKE.a mun yassare Alƙur'ani don wa'azantuwa da haddace-wa, to akwai mai wa'azantuwa da haddacewar?

(ƘISSAR MUTANEN ANNABI LUƊU ALAIHISSALAMU)

33. Haƙiƙa mutanen Annabi Luɗu sun ƙaryatada masu gargaɗi (wato da al'amura masu gargadi a kan harshen Annabi Luɗu alaihissalamu).
34. Haƙiƙa mu mun aiko iska a kan-su da take sheƙa musu ƙanƙananan tsakwankwani a kan fuskarsu suka halaka, sai iy-alin Annabi Luɗu (sune 'ya'yensa guda biyu), mun tser-ar dasu iokacin sahur).
35. Don ni'ima daga garemu kamar wancanenka sakamako ne muke sakawa wanda ya godewa ni'imominmu.
36. Haƙiƙa Annabi LucTu (alaihissa-lamu) ya tsoratar da su danS.armu (garesu), sai sukayi jayayya da gargaɗinmu.
37. Haƙiƙa sun yi nema ga baKinsa (wato ya barsu su gana dasu, saboda suyi mugun aiki dasu;ashe waɗannan Bala Mala'iku ne). Sai muka toshc idanuwan-su, (muka sanyata bada tsagi ba Jibrilu ne ya mari fuskokinsu da fiffikensa mukace dasu:) "Ku ɗanɗani azabatada gargaɗina".
38. Haƙiƙa azabata waye musu gari da sassafe (daga rana wacce ba a ayyana ba) azaba madauwa-miya mai saduwa da azabar la-hira.
39. (Za a ce dasu) "Ku cTandani azabatada gargaɗina".
40. Haƙiƙa mun yassare alƙur'ani saboda haddacewa to akwai mai haddacewa (don yagargadu?)
41. Haƙiƙa gargaɗi yazowa Fir'auna da mutanensa (bisa harshen Annabi Musa da Haru-na basu bada gaskiya ba).
42. Bari! sun ƙaryatada ayoyinmu dukkanta (wato guda tara wacce aka ba wa Annabi Musa) muka danlcensu da azabadanƙar ^aKƘarfa mai iko.

(BAN TSORO GA MUSHURIKAI TAREDA BAYANIN ARIBAR MASU TSORON ALLAH)

43. Shin kafiranku (ƙuraishu) su sukafi daga wadancan ababan ambato (Adu da Samudu ba ayi musu azaba ba?) ko kuna da kubuta ne daga azaba a cikin lit-tattafai. (Ya ku kafiran Ruraishu).
44. Bari! ko suna cewa: "Mu mndu-na ne masu farmaki (a kan An-nabi Sallallahu alaihi wa salla-ma yayin da Abu Jahil ya faɗi haka sai Ubangiji yace).
45. "Da sannu za ri ba wannan run-duna zasu girka aguje suna masu ba^da baya (an risbasu ra-nar Badar an taimaki manzon Allah (Shallallahu alaihi wa sal-' lama).
46. Bari! alƙiyama ce wurin alkaw-ari (nayi musu azaba) kuma alƙiyama tafi tsananin masifa, tafi azabar duniya (faci.
47. Haƙiƙa ma'abota laifi suna cikin halaka (a duniya da kisa) wuta abar hurawa (a lahira).
48. Ranar da ake jan su a cikin wuta giriri a kan fuskokinsu, ana ce dasu: "Ku ɗanɗani lasar Jahan-nama (gareku). **49.** Haƙiƙa mu kowane abu mun ha-licce shi ga gwargwado.

وَمَآ أَمۡرُنَآ إِلَّا وَٰحِدَةٞ كَلَمۡحِۭ بِٱلۡبَصَرِ ﴿50﴾ وَلَقَدۡ أَهۡلَكۡنَآ
أَشۡيَاعَكُمۡ فَهَلۡ مِن مُّدَّكِرٖ ﴿51﴾ وَكُلُّ شَيۡءٖ فَعَلُوهُ
فِي ٱلزُّبُرِ ﴿52﴾ وَكُلُّ صَغِيرٖ وَكَبِيرٖ مُّسۡتَطَرٌ ﴿53﴾ إِنَّ ٱلۡمُتَّقِينَ
فِي جَنَّٰتٖ وَنَهَرٖ ﴿54﴾ فِي مَقۡعَدِ صِدۡقٍ عِندَ مَلِيكٖ مُّقۡتَدِرِۭ ﴿55﴾

55 سُورَةُ الرَّحۡمَٰنِ مَدَنِيَّة

وَهِيَ سَبۡعٌ وَسَبۡعُونَ ءَايَة 77

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

* ٱلرَّحۡمَٰنُ عَلَّمَ ٱلۡقُرۡءَانَ ﴿1﴾ خَلَقَ ٱلۡإِنسَٰنَ عَلَّمَهُ ٱلۡبَيَانَ ﴿2﴾ حزب
ٱلشَّمۡسُ وَٱلۡقَمَرُ بِحُسۡبَانٖ ﴿3﴾ وَٱلنَّجۡمُ وَٱلشَّجَرُ يَسۡجُدَانِ ﴿4﴾
وَٱلسَّمَآءَ رَفَعَهَا وَوَضَعَ ٱلۡمِيزَانَ ﴿5﴾ أَلَّا تَطۡغَوۡاْ فِي ٱلۡمِيزَانِ ﴿6﴾
وَأَقِيمُواْ ٱلۡوَزۡنَ بِٱلۡقِسۡطِ وَلَا تُخۡسِرُواْ ٱلۡمِيزَانَ ﴿7﴾ وَٱلۡأَرۡضَ
وَضَعَهَا لِلۡأَنَامِ ﴿8﴾ فِيهَا فَٰكِهَةٞ وَٱلنَّخۡلُ ذَاتُ ٱلۡأَكۡمَامِ ﴿9﴾
وَٱلۡحَبُّ ذُو ٱلۡعَصۡفِ وَٱلرَّيۡحَانُ ﴿10﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿11﴾
خَلَقَ ٱلۡإِنسَٰنَ مِن صَلۡصَٰلٖ كَٱلۡفَخَّارِ ﴿12﴾ وَخَلَقَ
ٱلۡجَآنَّ مِن مَّارِجٖ مِّن نَّارٖ ﴿13﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿14﴾

50. Umarninmu ga wani abu (da muke nufin samar dashi) bai kasance ba illa umarni guda ɗaya, kamar Iciftawa da ido sai a sami abin. Haƙiƙa al'amarinsa idan yanufi wani abu sai yace "samu" saiya samu).
51. Haƙiƙa mun halakar da maka-mantanku a cikin kafirci na daga al'umma gabanku wacce ta wuce), to yalla akwai mai gargaduwa?
52. Kowane abu da bayi suka aika-ta, an rubutashi a cikin littafi (na mahardata Mala'iku).
53. Dukkan ƙanƙani ko babbana daga zunubi yana mbuce (a Lauhil Mahafuzu).
54. Haƙiƙa masu tsoron Allah suna cikin aljannatai da ƙoramu.
55. A mazaunin mutanen gaskiya, nan ga gawurtaccen Sarki mai yawan iko (Shine Allah wato kusancin falala da girma).

Wannan sura Itace Suratu Arrahmanu Azza wa Jallah

A Makka aka saukar da ita Aya Saba'in da bakwai ce (77)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, nai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe

(Wannan sura ta leunshi anbaton Alƙur'ani wandaShine mafi gir-man ni'ima bisa mutum, sannan ni'imomi na kasancewa a cikin sammai da ƙassai, sannan halit-tar mutum da aljan, sannan sifar alfdyama da matsayin mutane a cikintada bayanin Aljanna da wutada abinda yake cikinsu).

(UWAYEN NI'IMOMI ITACE AMARYAR ALƘUR'ANI)

1. Ubangiji mai yawan rahama yasanar da (wanda yaga dama) Alƙur'ani.
2. Ya halicci dukkan dan Adam, yasanar dashi bayani (Shine furu-ci Annabi Muhammadu SallAllahu alaihi wa sallama; yasanar dashi abinda ya kasance da wandazai kasance don Shine Al-insanul Kamilu, mutum ci-kakke wanda yake Shine ma-baiyanar Alƙur'ani (Shehu Ab-dulKarimuljilani ya tsaya da wannan bayani a cikin littafinsa da ake kiransa AL-INSANIL KA-MIL, Malam ne yayi wannan bayani.)
3. Rana da wata suna gudana da lis-safi.
4. Wato najamu, tsiri mai yacTo da Itace mai tsaiwa a kan malcengyamarsa suna sujada ga Allah.
5. Sama ya daukakata ya kafa adal-ci.
6. Don kada kuyi zalinci a ma'auni.
7. Ku tsaida awo da adalci, kadaku ,tauye abin aunawa (mizani a biyu abin awo dashi wato ka-mar dan dutse mizani na uku abin aunawa).
8. ƙasa ya tabbatar da ita saboda halitta (mutum da aljan da wa-ninsu).
9. Abin marmari na cikinta, da da-bino ma'abocin kwasfanni.
10. Da Kwaya (kamar alkama da sha'ir da makamantansu), ma'abocin Kaiƙayi, da ganye mai Kanshi.
11. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryatawa dashi? (Yaku aljanu da mutane. An ambaci wannan aya sau tala-tin da ɗaya, tambayo a cikinta saboda tabbatarwa ne. (SHASHIN NI'IMOMIN UBANGIJI)
12. Ubangiji ya halicci Annabi Ada-mu daga yunBu Kdcashashshe, (mai amo idan an lcwanlcwasa shi) kamar kasko dafaffe.
13. Ya halicci Iblis daga tatacce na harshen wuta.
14. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryatawa? (Ban mu ƙaryatada ko ɗayabaya Ubangiji).

رَبُّ الْمَشْرِقَيْنِ وَرَبُّ الْمَغْرِبَيْنِ ﴿15﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿16﴾
مَرَجَ الْبَحْرَيْنِ يَلْتَقِيَانِ ﴿17﴾ بَيْنَهُمَا بَرْزَخٌ لَّا يَبْغِيَانِ ﴿18﴾
فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿19﴾ يَخْرُجُ مِنْهُمَا اللُّؤْلُؤُ وَالْمَرْجَانُ ﴿20﴾
فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿21﴾ وَلَهُ الْجَوَارِ الْمُنشَئَاتُ فِي الْبَحْرِ كَالْأَعْلَامِ ﴿22﴾
فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿23﴾ كُلُّ مَنْ عَلَيْهَا فَانٍ ﴿24﴾ وَيَبْقَىٰ وَجْهُ
رَبِّكَ ذُو الْجَلَالِ وَالْإِكْرَامِ ﴿25﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿26﴾
يَسْـَٔلُهُ مَن فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ كُلَّ يَوْمٍ هُوَ فِي شَأْنٍ ﴿27﴾
فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿28﴾ سَنَفْرُغُ لَكُمْ أَيُّهَ الثَّقَلَانِ ﴿29﴾
فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿30﴾ * يَا مَعْشَرَ الْجِنِّ وَالْإِنسِ إِنِ اسْتَطَعْتُمْ
أَن تَنفُذُوا مِنْ أَقْطَارِ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ فَانفُذُوا لَا تَنفُذُونَ إِلَّا بِسُلْطَانٍ ﴿31﴾
فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿32﴾ يُرْسَلُ عَلَيْكُمَا شُوَاظٌ مِّن نَّارٍ ﴿33﴾
وَنُحَاسٌ فَلَا تَنتَصِرَانِ ﴿34﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿35﴾
فَإِذَا انشَقَّتِ السَّمَآءُ فَكَانَتْ وَرْدَةً كَالدِّهَانِ ﴿36﴾
فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿37﴾ فَيَوْمَئِذٍ لَّا يُسْـَٔلُ عَن
ذَنۢبِهِۦٓ إِنسٌ وَلَا جَآنٌّ ﴿38﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿39﴾

ثمن

15. Ubangijin mahudar rana guda biyu (na dari dana damina),kuma Ubangijin mafadar rana (na dari dana damina).
16. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryatawa? (Ban mu ƙaryatada ko ɗayabaya Ubangiji).
17. Ya saki koguna biyu (na dadi dana zartsi), suna ganuwa a ganin ido.
18. Akwai shamakin (ikon Allah) tsakaninsu basa zalinci ga ju-nansu, (wato basa cudanya).
19. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kiike ƙaryatawa? (Bamu _aryatada ko ɗayabaya Ubangijinmu).
20. Ana fitar da lu'ulu'u da murjani daga garesu (wato daga matatta-rinsu, mai gasgatada dayansu).
21. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku baku bada gaskiya ba? (Babu ɗaya daga ni'imominsa da bamu bada gaskiya dasu baya Ubangiji).
22. Jiraga ababan fararwa a kogi ka-mar duwarwatsu (a girma da tudu na Ubangiji ne).
23. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku baku bada gaskiya ba? (Babu ɗaya daga ni'imomin Ubangijinmu wanda bamu bada gaskiya dashi da, Ya Ubangijinmu).
24. Dukkan wanda yake bayan ¯asa Rararre ne.
25. Zatin Ubangijinka ne yake wan-zuwa, ma'abocin girma da alhe-ri (ga muminai da ni'imominsa a garesu).
26. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku baku bada gaskiya ba? (Babu ɗaya daga ni'imomin wanda bamu bada gaskiya dashi ba, Ya Ubangi-jinmu).

(WANI ABU DAGA NI'IMOMIN ALLAH RANAR ALƘIYAMA)

27. Wanda yake sammai da ƙassai yana bara ga Ubangiji, (abinda yake bukata na Karfi kan ibada da arziki da gafara da wanin wannan). Kowane lokaci shi Ubangiji yana cikin sha'ani (a bisa daidai da abinda ya Kaddara shi a azal na daga rayawa da kashewa da girmama wa da wulaƙantawa da wadatawa da talautawa da amsa roKo da baiwa mai tambayo da wanin wannan).
28. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku baku bada gaskiya ba, (yaku bayi, babu abinda bamu bada gaskiya dashi baya Ubangijinmu).
29. Da sannu zamuyi nufi dayi muku sakamako yaku manyan halitta guda biyu, mutum da al-jan.
30. Da wanne abu ne daga ni'imomin Ubangijinkune baku bada gaskiya ba? (Babu abinda bamu bada gaskiya dashi bana ni'imominka Ya Ubangi-jinmu).
31. Yaku jama'ar Aljanu da Mu-tane in kuka sami damar ku fita daga sassan sammai da ƙassai to ku fita, bazaku fita basaida Karfi (namu, ba ƙarfi gareku a kan wannan. Wannan umarni bana ta'ajizi bane, kamar yadda aka sa a cikin fassara, umarnine na halattawa ko mandubantawa,don an sami zarcewa a cikin samman da ƙassan a yau).
32. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku baku bada gaskiya ba? (Babu wani abu daga ni'imomin Ubangijinmu da bamu bada gaskiyabaya Ubangi-jinmu).
33. Ana sakowar tartsatsi na wuta a kanku.
34. Da hayaki maras harshe, bazaku hanu ga buran wannan ba, (bari! zai kora kune izuwa tar-on alƙiyama).
35. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku baku bada gaskiya ba? (Babu ɗaya da bamu bada gaskiyabaya Ubangijin-mu).
36. A yayin da sama ta kyarkecc kofa Kofa (to yaya mana kin abinda ya girmama razani a wannan ransa?) Shine ta zama jazur kamar fata ja sabanin yad-da take a da.
37. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku baku bada gaskiya ba? (Babu ɗaya daga ni'imar Ubangijinmu da bamu bada gaskiyabaya Ubangijin-mu)."
38. A wannan rana ne baza a tam-bayi mutum ko aljan da laifin dayayi ba, (za a tambayesu a wani lokaci daban).
39. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku baku bada gaskiya ba?

يُعْرَفُ الْمُجْرِمُونَ بِسِيمَاهُمْ فَيُؤْخَذُ بِالنَّوَاصِي وَالْأَقْدَامِ ﴿40﴾
فَبِأَيِّ آلَاءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿41﴾ هَٰذِهِ جَهَنَّمُ الَّتِي يُكَذِّبُ بِهَا الْمُجْرِمُونَ ﴿42﴾
يَطُوفُونَ بَيْنَهَا وَبَيْنَ حَمِيمٍ آنٍ ﴿43﴾ فَبِأَيِّ آلَاءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿44﴾
وَلِمَنْ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِ جَنَّتَانِ ﴿45﴾ فَبِأَيِّ آلَاءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿46﴾
ذَوَاتَا أَفْنَانٍ ﴿47﴾ فَبِأَيِّ آلَاءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿48﴾
فِيهِمَا عَيْنَانِ تَجْرِيَانِ ﴿49﴾ فَبِأَيِّ آلَاءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿50﴾
فِيهِمَا مِنْ كُلِّ فَاكِهَةٍ زَوْجَانِ ﴿51﴾ فَبِأَيِّ آلَاءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿52﴾
مُتَّكِئِينَ عَلَىٰ فُرُشٍ بَطَائِنُهَا مِنْ إِسْتَبْرَقٍ وَجَنَى الْجَنَّتَيْنِ دَانٍ ﴿53﴾
فَبِأَيِّ آلَاءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿54﴾ فِيهِنَّ قَاصِرَاتُ الطَّرْفِ
لَمْ يَطْمِثْهُنَّ إِنْسٌ قَبْلَهُمْ وَلَا جَانٌّ ﴿55﴾ فَبِأَيِّ آلَاءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿56﴾
كَأَنَّهُنَّ الْيَاقُوتُ وَالْمَرْجَانُ ﴿57﴾ فَبِأَيِّ آلَاءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿58﴾
ربع * هَلْ جَزَاءُ الْإِحْسَانِ إِلَّا الْإِحْسَانُ ﴿59﴾ فَبِأَيِّ آلَاءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿60﴾
وَمِنْ دُونِهِمَا جَنَّتَانِ ﴿61﴾ فَبِأَيِّ آلَاءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿62﴾
مُدْهَامَّتَانِ ﴿63﴾ فَبِأَيِّ آلَاءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿64﴾
فِيهِمَا عَيْنَانِ نَضَّاخَتَانِ ﴿65﴾ فَبِأَيِّ آلَاءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿66﴾

40. Ana sanin masu laifi da alamo-minsu ayi danka da makwark-wadarsu (gashin goshinsu) da dugaduggansu (wato za a tara makwarkwadarsu da dugadu-gansu ajefa wuta ta baya).
41. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku baku bada gaskiya ba?
42. Wannan jahannama ce wacce masu laifi suke ƙaryatata.
43. Suna yin kewayo tsakanintada tsakanin ruwan zafi (in sun nemi taimako da zafin wutar ja-hannama).
44. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku baku bada gaskiya ba? (Babu daya da bamu bada gaskiya da sbi baya Ubangiji).
(DAGA NPIMOMIN UBANGIJI GA MASU TSORON ALLAH RANAR ALƘIYAMA)
45. Aljanna guda biyu sun tabbata ga dukkan wanda yaji tsoron tsaiwarsa nan gaba ga Ubangiji, saboda hisabi yabar sabonsa (Aljanna guda biyu ɗaya ta Shu-hudı ce a duniyaganin zuci, ta biyu Jannatul Firdausi ce da gani da ido a Lahira).
46. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryatawa? (Bamu ƙaryata ko ɗaya daga ni'imominka baya Ubangiji).
47. Ma'abuta rassa guda biyu (wato kowane reshe ya tattara bisa ga-nye da 'ya'yan itaciya).
48. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku baku bada gaskiya ba? (Ban mu ƙaryatada ko cTayabaya Ubangijinmu).
49. Akwai idanuwa guda biyu suna kwarara a cikinsu.
50. Daga Wanne ce daga ni'imomin Ubangijinku kuke learyatawa? (Bamu ƙaryatada ko ɗayabaya Ubangijinmu).
51. Akwai nau'i guda biyu a cikinsu na daga dukkan kayan marmari (da danye da ƙeƙasheshshe, mai daci daga cikinsu a duniya ka-mar guna mai zaki a can).
52. To daga wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryatawa? (Bamu ƙaryatada ko ɗayabaya Ubangijinmu).
53. Suna more dadi halin kasance-warsu, suna jingine a kan shinfiɗu wato katifu waɗanda jaku-nansu cikinsu na istabraƙu ne (wato kakkauran dibajc kakkau-sa. Zaha'iru kuma rigunan mat-asan kan Furushun wato katifu) abindasa na aljannar guda biyu, (wato 'ya'yan itaciyarsu) maku-sanci ne, (ana tsinkarsu daga tsaye ko kwance ko zaune.)
54. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryatawa? (Bamu ƙaryatada ko ɗayabaya Ubangijinmu).
55. A cikin waɗannan aljannatai da abinda suka ƙunsa na daga be-naye da gidaje akwai yan mata masu taƙaitawan kallonsu a kan mazajensu wani mutum gabansu bai taɓa shafar su ba wala wani aljan.
56. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryatawa? (Bamu ƙaryatada ko ɗayabaya Ubangijinmu).
57. Kai kace su mutanen nan Yaƙutu ne ai su tsarkaka ne ga buran Rura da daudakai kace su) marjanine (ai su kamar lu'ulu'u ne a fari).
58. To da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryata wa? (Ban mu ƙaryatada ko ɗayabaya Ubangijinmu).
59. Babu wani sakamako na da'a sai kyautatawa da ni'ima. (Ihasni Shine ka bautawa Allah kamar kana ganinsa, Illal ihsanu Shine ya ni'imtaka da ganin zatinsa da idanuwanke.)
60. To da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryatawa? (Bamu ƙaryatada ko ɗaya da ni'imominka baya Ubangijin-mu).
(DAGA NI'IMOMINSA BISA MUMINAI RANAR ALƘIYAMA)
61. A koma baya da waɗancananka aljanna guda biyu da aka ambata, akwai aljanna guda biyu ga wanda yaji tsoron tsaiwa gaban Ubangijinsa din, (amma tsoron bai kai kamar tsoron farko ba. Saboda shi yana da ɗa'a a mat-sayin Ubangiji yana ganinsa.)
62. Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryatawa? (Bamu ƙaryatada ko ɗayabaya Ubangijinmu).
63. Masu baƙi saboda tsananin kore,

فِيهِمَا فَاكِهَةٌ وَنَخْلٌ وَرُمَّانٌ ﴿67﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿68﴾
فِيهِنَّ خَيْرَاتٌ حِسَانٌ ﴿69﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿70﴾
حُورٌ مَّقْصُورَاتٌ فِي الْخِيَامِ ﴿71﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿72﴾
لَمْ يَطْمِثْهُنَّ إِنسٌ قَبْلَهُمْ وَلَا جَآنٌّ ﴿73﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿74﴾
مُتَّكِـِٔينَ عَلَىٰ رَفْرَفٍ خُضْرٍ وَعَبْقَرِيٍّ حِسَانٍ ﴿76﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿75﴾
تَبَٰرَكَ اسْمُ رَبِّكَ ذِي الْجَلَٰلِ وَالْإِكْرَامِ ﴿77﴾

سُورَةُ الْوَاقِعَةِ مَكِّيَّةٌ 56
وَهِيَ تِسْعٌ وَتِسْعُونَ ءَايَةً 99

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

إِذَا وَقَعَتِ الْوَاقِعَةُ ﴿1﴾ لَيْسَ لِوَقْعَتِهَا كَاذِبَةٌ ﴿2﴾ خَافِضَةٌ رَّافِعَةٌ ﴿3﴾
إِذَا رُجَّتِ الْأَرْضُ رَجًّا ﴿4﴾ وَبُسَّتِ الْجِبَالُ بَسًّا ﴿5﴾ فَكَانَتْ هَبَآءً
مُّنۢبَثًّا ﴿6﴾ وَكُنتُمْ أَزْوَاجًا ثَلَٰثَةً ﴿7﴾ فَأَصْحَٰبُ الْمَيْمَنَةِ ﴿8﴾ مَا أَصْحَٰبُ
الْمَيْمَنَةِ ﴿9﴾ وَأَصْحَٰبُ الْمَشْـَٔمَةِ ﴿10﴾ مَا أَصْحَٰبُ الْمَشْـَٔمَةِ ﴿11﴾ وَالسَّٰبِقُونَ
السَّٰبِقُونَ ﴿12﴾ أُوْلَٰٓئِكَ الْمُقَرَّبُونَ ﴿13﴾ فِي جَنَّٰتِ النَّعِيمِ ﴿14﴾ ثُلَّةٌ مِّنَ الْأَوَّلِينَ ﴿15﴾ وَقَلِيلٌ
مِّنَ الْآخِرِينَ ﴿16﴾ عَلَىٰ سُرُرٍ مَّوْضُونَةٍ ﴿17﴾ مُّتَّكِـِٔينَ عَلَيْهَا مُتَقَٰبِلِينَ ﴿18﴾

64. Da wanne ne daga ni'imomm Ubangijinku baku bada gaskiya dashi ba? (Babu ɗaya daga ni'imomin da bamu bada gaskiya dashi ba). **65.** Akwai idanuwa guda biyu a cikinsu masu tsugo da ruwa basa tsagaitawa. **66.** To da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryatawa? (Bamu ƙaryatada ko ɗayabaya Ubangijinmu). **67.** Akwai kayan marmari a cikinsu da dabino da mmmani. **68.** Da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryata wa? (Bamu ƙaryatada ko ɗayabaya Ubangijinmu). **69.** A cikin aljannatan guda biyu akwai 'yanmata mafifita (a wajen tadodi) kyawawa (a fuskokinsu). **70.** To da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kukc fcaryatawa? (Bamu ƙaryatada ko ɗayabaya Ubangijinmu). **71.** Masu tsananin bakin kwaranyar idaniya da tsananin farinta aba-ban boyewa a cikin laimomi (na lu'ulu'u rarakakke a cike da gi-daddajin, wannan lu'ulu'i ya zama kamar mayafi a garesu. **72.** To da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryatawa? (Bamu ƙaryatada ko ɗayabaya Ubangijinmu).

73. Wani mutum gaban mazajcnsu ko aljan bai taɓa shafar su ba.

74. To da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryatawa? (Bamu ƙaryatada ko ɗayabaya Ubangijinmu).

75. Suna jin dadi suna lilo a kan ga-daje korra da dardumomi kya-wawa.

76. To da wanne ne daga ni'imomin Ubangijinku kuke ƙaryatawa? (Bamu ƙaryatada ko ɗayabaya Ubangijinmu).

77. Sunan Ubangijinka ma'abocin girma da Ikrami (Taƙasara Khairuhu Wa Ta'zayada, Mal-am yace saboda kasancewar su masu wannan aljanna masu muraRabane a duniya, 'yan ta-jallin asma'u ne da sifofi wacTancan na farko a duniya yan tajallin zati ne).

Wannan sura Itace Suratul Waki'ati

A Makka aka saukar da ita Aya casa'in da tara ce (99)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, nai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe

Wannan Sura Manzon Allah SallAllahu alaihi wa sallama yana am-batonta Suratul GINA yana cewa ku karanta ta ku sanar da 'ya'yanku ita. Ta tattara a kan Alƙiyama da Haluluwanta, san-nan bayanin abinda Allah ya tanadar ga masu tsere da Asha-bul Yamini da abinda aka tana-da ga Ashabushshimali a wuta, sannan ambaton Halittar mu-tum, da tsiri da ruwa da wutada ambaton taurari da ma'auni da wanin wancanenka na daga dal-ilan ikon Allah).

TASHIN ALƘIYAMA

1. Idan alƙiyama ta tashi. **2.** Babu wata kai mai ƙaryatawa ga tashinta, (tamfar data ƙaryata a duniya). **3.** (Itace) mai kaskastawa (ga wadansu mutane dashigarsu wuta). Mai daukakawa (ga wadansu dashigarsu aljanna). **4.** Idan aka girgiza ƙasa girzawa. **5.** Aka dandake duwarwatsu dan-daKewa. **6.** Ta zama Kurar taga abar sheKewa.

(WAƊANNAN SUNE MARIGAYAKUMA GA SAKAMAKONSU)

7. Idan kuka kasance (a cikin alƙiyama) dangogi guda uku. **8.** To ma'abota dama (waɗanda ake basu littafinsu da hannun dama). **9.** Wane abu ne ma'abota dama? (Don girmama wa ga sha'aninsu saboda shiga aljanna). **10.** Da ma'abota hagun (waɗanda ake basu takardarsu a hagu). **11.** Wane abu ne ma'abota hagun? (Don wulakantarwa ga sha'aninsu dashiga wuta). **12.** Da masu tsere (Izuwa alheri An-nabawa sune haƙiƙa nin) masu tsere (don girmama wa ga sha'aninsu, labarin Wassa-biƙuna Shine). **13.** Wadancanenka sune haƙiƙa nin ababan kusantawa. **14.** Suna cikin aljannarjin dadi.

15. Jama'a ne masu yawa daga mu-tanen farko (sune Sahabban Manzon Allah Sallallahu alaihi wa sallama daga mutanen farko izuwa ƙarshen ƙami na uku).

16. Da kaɗan daga mutanen Rarshe (na wannan izuwa tashin alƙiyama).

17. Suna kan gadaje abin sakewa da lu'ulu'anya da zinari (a maRabilin gadaje da ake sake su da igiya wanda Larabawa suke cewa dashi (Anƙarib, Malam ne ya faɗa.)

18. Suna dogare a kanta, halin ka-sancewarsu su suna kallon juna.

يطوف عليهم ولدان مخلدون ﴿19﴾ بأكواب وأباريق وكأس من معين ﴿20﴾
لا يصدعون عنها ولا ينزفون ﴿21﴾ وفاكهة مما يتخيرون ﴿22﴾
ولحم طير مما يشتهون ﴿23﴾ وحور عين ﴿24﴾ كأمثال اللؤلؤ المكنون ﴿25﴾
جزاء بما كانوا يعملون ﴿26﴾ لا يسمعون فيها لغوا ولا تأثيما
إلا قيلا سلاما سلاما ﴿27﴾ * وأصحاب اليمين ﴿28﴾ ما أصحاب اليمين ﴿29﴾ ثمن
في سدر مخضود ﴿30﴾ وطلح منضود ﴿31﴾ وظل ممدود ﴿32﴾ وماء
مسكوب ﴿33﴾ وفاكهة كثيرة ﴿34﴾ لا مقطوعة ولا ممنوعة ﴿35﴾
وفرش مرفوعة ﴿36﴾ إنا أنشأناهن إنشاء ﴿37﴾ فجعلناهن
أبكارا ﴿38﴾ عربا أترابا ﴿39﴾ لأصحاب اليمين ﴿40﴾ ثلة من الأولين ﴿41﴾
وثلة من الآخرين ﴿42﴾ وأصحاب الشمال ﴿43﴾ ما أصحاب الشمال ﴿44﴾
في سموم وحميم ﴿45﴾ وظل من يحموم ﴿46﴾ لا بارد ولا كريم ﴿47﴾
إنهم كانوا قبل ذلك مترفين ﴿48﴾ وكانوا يصرون على
الحنث العظيم ﴿49﴾ وكانوا يقولون أئذا متنا وكنا ترابا
وعظاما إنا لمبعوثون ﴿50﴾ أو آباؤنا الأولون ﴿51﴾ قل إن
الأولين والآخرين ﴿52﴾ لمجموعون إلى ميقات يوم معلوم ﴿53﴾

19. Samari suna kewayo a kansu sa-boda hidima, abadan dauwamarwa kan kuruciyarsu bazasu tsufa ba.
20. Suna kewayo da finjaloli da sin-tala ko bardadu.
21. Da gidauniya ta marmaro mai gudana (wato giyar Aljanna, wanda bazata yanke ba har abada).
22. Basa yin ciwon kai saboda ita wannan giya basa yin maye.
23. Da abin marmari daga abinda suke zabi.
24. Da naman tsuntsu daga abinda suke marmari.
25. Suna da mata masu tsananin far-in idaniya, bakin idaniya da fa-rinta, masu gada-gadan idaniya kai kace lu'ulu'u ne abin boyewa.
26. (Mun sanya wancanenka garesu) don sakamako na daga abinda suka kasance suna aikatawa.
27. Basa jin alfasha a cikin aljanna, (wato basa yin mummunan zance don abincinsu a duniya zikirillahi), wala daukar zunubi (akayi musu sakamako mai da-cewa da abinda suka aikata).
28. Saidai magana salamun-salamun.(Waɗannan sune masu Ihsani a matsayin masu bautawa Allah kamar suna ganinsa wato ma'abota Dama da Sakamakon-su).
29. Wane abu ne ma'abota dama? Abu ne babba ma'abota dama.
30. Suna cikin magarya maras Kaya.
31. Da ayaba abar dbdɗorawa.
32. Da inuwa madawwamiya.
33. Da ruwa mai kwarara.
34. Da kayan marmari mai yawa.
35. Ba abar yankewa (a zamani) ba, wata abar hanawa (da wani abu badaga garesu ko ƙayako wani abu wandazai hana tsinka.)
36. Dashinfidu ababan shinfidawa a kan gado.
37. Mu mun kagesu kagowa (ba tareda haihuwa ba,) saboda ma'abota dama.
38. Mu mun sanya su 'yan mata (wato kodayaushe mazajensu sukazo musu saisu samesu da budurci ba tareda zafi ba),
39. Masu soyayya izuwa mazajensu kuma tsareku, (wato masu she-karu iri ɗaya.)
40. Na ma'abota dama, wato (sune masu bautar Allah kamar suna ganinsa).
SUMUNI
41. Su jama'a ce masu yawa na mu-tanen farko.
42. Da jama'a masu yawa na muta-nen karshe.
(WArfANNAN SUNE 'YAN HAGU WANNAN KUMA SHINE SAKAMAKONSU)
43. Ma'abuta hauni.
44. Abu ne wulakantacce ma'abuta hagu.
45. Suna cikin iska mai tsananin zafi ta wutada take shiga cikin katofin gashi.
46. Da inuwa ta baƙin hayaƙi.
47. Ba mai sanyi ba (kamar waninsa na daga inuwoyi,) ba mai kyan ganiba.
48. Haƙiƙa haƙiƙa sun kasance gaban wan-canenka (a duniya) ababan ni'imtawa, basa wahalar da kansu cikin da'ar Ubangiji.
49. Sun kasance suna zarcewa a cikin zunubi mai girma wato shurka da Ubangiji.
50. Sun kasance suna faɗi "yanzu idan mun mutu mun kasance turbaya da kasusuwa, shin haƙiƙa mu lallai za a tashemu?".
51. "Ko iyayenmu na farko?".
52. Cen haƙiƙa mutanen farko dana karshe ababan tarawa ne (ranar Al□iyama).
53. Izuwa lokacin rana abin sani (Shine alƙiyama).

ثُمَّ إِنَّكُمْ أَيُّهَا الضَّآلُّونَ الْمُكَذِّبُونَ ﴿54﴾ لَأٓكِلُونَ مِن شَجَرٍ
مِّن زَقُّومٍ ﴿55﴾ فَمَالِـُٔونَ مِنْهَا الْبُطُونَ ﴿56﴾ فَشَارِبُونَ عَلَيْهِ مِنَ
الْحَمِيمِ ﴿57﴾ فَشَارِبُونَ شُرْبَ الْهِيمِ ﴿58﴾ هَٰذَا نُزُلُهُمْ يَوْمَ الدِّينِ ﴿59﴾
نَحْنُ خَلَقْنَٰكُمْ فَلَوْلَا تُصَدِّقُونَ ﴿60﴾ أَفَرَأَيْتُم مَّا تُمْنُونَ ﴿61﴾
ءَآنتُمْ تَخْلُقُونَهُۥ أَمْ نَحْنُ الْخَٰلِقُونَ ﴿62﴾ نَحْنُ قَدَرْنَا بَيْنَكُمُ الْمَوْتَ
وَمَا نَحْنُ بِمَسْبُوقِينَ ﴿63﴾ عَلَىٰ أَن نُّبَدِّلَ أَمْثَٰلَكُمْ وَنُنشِئَكُمْ
فِي مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿64﴾ وَلَقَدْ عَلِمْتُمُ النَّشْأَةَ الْأُولَىٰ فَلَوْلَا تَذَّكَّرُونَ ﴿65﴾
أَفَرَأَيْتُم مَّا تَحْرُثُونَ ﴿66﴾ ءَآنتُمْ تَزْرَعُونَهُۥ أَمْ نَحْنُ الزَّٰرِعُونَ ﴿67﴾
لَوْ نَشَآءُ لَجَعَلْنَٰهُ حُطَٰمًا فَظَلْتُمْ تَفَكَّهُونَ ﴿68﴾ إِنَّا لَمُغْرَمُونَ ﴿69﴾
بَلْ نَحْنُ مَحْرُومُونَ ﴿70﴾ أَفَرَأَيْتُمُ الْمَآءَ الَّذِي تَشْرَبُونَ ﴿71﴾
ءَآنتُمْ أَنزَلْتُمُوهُ مِنَ الْمُزْنِ أَمْ نَحْنُ الْمُنزِلُونَ ﴿72﴾ لَوْ نَشَآءُ
جَعَلْنَٰهُ أُجَاجًا فَلَوْلَا تَشْكُرُونَ ﴿73﴾ أَفَرَأَيْتُمُ النَّارَ الَّتِي تُورُونَ ﴿74﴾
ءَآنتُمْ أَنشَأْتُمْ شَجَرَتَهَا أَمْ نَحْنُ الْمُنشِـُٔونَ ﴿75﴾ نَحْنُ جَعَلْنَٰهَا
تَذْكِرَةً وَمَتَٰعًا لِّلْمُقْوِينَ ﴿76﴾ فَسَبِّحْ بِاسْمِ رَبِّكَ الْعَظِيمِ ﴿77﴾
* فَلَا أُقْسِمُ بِمَوَٰقِعِ النُّجُومِ ﴿78﴾ وَإِنَّهُۥ لَقَسَمٌ لَّوْ تَعْلَمُونَ عَظِيمٌ ﴿79﴾ ربع

54. Sannan haƙiƙa ku yaku wađannan batattu masu ƙaryatawa.
55. Lallai masu ci ne daga cikin Itace na Zaloimu, (wato mafi munin itatuwan ne ana samunsa a cikin ƙasashen Hijaz).
56. To zasu cika cikinsu da ita mummunan itaciya.
57. Zasu kwankwadi ruwan zafi a kansa.
58. Zasu dinga shansa irin yadda raƙuma masu tsananin Kishirwa zasu rinka shansa.
59. Wannan Shine garar baƙinsu (Liyafarsu) a ranar sakamako (wato ranar alƙiyama).

(BA'ALIN DALILAI A KAN TABBATAR DA IKON ALLAH A KAN TASHIN ALƘIYAMA DA WANINSA)

60. Mune muka halicceku (wato muka samar daku ,daga rashi), saboda me baku gasgatada ta-shin alƙiyama ba? (Don mai ikon ya farar bayan babu wato Shine Insha'i, mai ikone bisa mayarwa).
61. Shin ku bamu labari, abinda kuke zubawa maniyi a cikin ma-haifar mata?
62. Shin kune kuke halittarsa (ya zama mutum) ko mune muke halittarsa?
63. Mune muka kaddara mutuwa tsakaninku mu ba masu gajiy-awa bane.
64. A kan mu zoda misalce-misalcenku a maimakonku. Kuma mu halicceku cikin abinda baku sani ba (kamar birrai da alhinzirai).
65. Haƙiƙa kun san tashi na farko, saboda me baku wa'azantu ba? Me ya hana ku wa'azantuwa.
66. Shin ku bamu labarin abinda kuke nomawa (wato □asa da kuke binne iri cikinta?).
67. Shin kune kuke tsiro dashi? Ko mune muke tsiro dashi? (Ubangiji kai ne).
68. Da mun ga dama da mun mai dashi busashshen yayi, sai ku zamo kuna mana ki (daga wan-nan).
69. Kuna cewa; mu ababan halakar-wa ne (saboda arzikinmu ya ha-laka).
70. Bari! mu ababan haramtawa ne daga arzikmmu.
71. Shin ku bamu labarin ruwan da kuke sha.
72. Shin kune kuka saukar dashi daga gizagizai? Ko mune muka saukar dashi? (Ubangiji kai ne).
73. Da mun ga dama da mun sanyashi ruwan gishiri (da baza a iya shan sa ba,) to dan me baku go-dewa (ni'imata ba?).
74. Shin ku bamu labarin wuta, wacce kuke kyastawa daga Itace kore.
75. Shin kune kuka fari itaciyarta? (Kamar turgunuwa da tumfafiya da tafasa. An mbuto daga ibn Abbasin cewa shi yace, "babu daga bishiya wala ƙe, face akwai wuta cikinsa sai nama-nama) ko ko mune masu farar da ita? (Ubangiji kai ne).
76. Mune muka sanyata gargađi (ga wutar Jahannama) da jin dadi ga matafiya.
77. To ka tsarkake sunan Ubangijin-ka mai girma (Ance ismu za'idi ne to baza'idi ne ba).

(WANNAN LALLAI SHINE HAkkUL YAƘINU)

78. Ina rantsuwa da mafadan nan na taurari.
79. Haƙiƙa shi rantsuwa da ita lallai rantsuwa ce mai girma da kun san girman wannan rantsuwa.

إِنَّهُۥ لَقُرْءَانٌ كَرِيمٌ ﴿٧٧﴾ فِي كِتَٰبٍ مَّكْنُونٍ ﴿٧٨﴾ لَّا يَمَسُّهُۥٓ إِلَّا ٱلْمُطَهَّرُونَ ﴿٧٩﴾
تَنزِيلٌ مِّن رَّبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٨٠﴾ أَفَبِهَٰذَا ٱلْحَدِيثِ أَنتُم مُّدْهِنُونَ ﴿٨١﴾ وَتَجْعَلُونَ
رِزْقَكُمْ أَنَّكُمْ تُكَذِّبُونَ ﴿٨٢﴾ فَلَوْلَآ إِذَا بَلَغَتِ ٱلْحُلْقُومَ ﴿٨٣﴾ وَأَنتُمْ
حِينَئِذٍ تَنظُرُونَ ﴿٨٤﴾ وَنَحْنُ أَقْرَبُ إِلَيْهِ مِنكُمْ وَلَٰكِن لَّا تُبْصِرُونَ ﴿٨٥﴾
فَلَوْلَآ إِن كُنتُمْ غَيْرَ مَدِينِينَ ﴿٨٦﴾ تَرْجِعُونَهَآ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٨٧﴾ فَأَمَّآ إِن
كَانَ مِنَ ٱلْمُقَرَّبِينَ ﴿٨٨﴾ فَرَوْحٌ وَرَيْحَانٌ وَجَنَّتُ نَعِيمٍ ﴿٨٩﴾ وَأَمَّآ إِن كَانَ
مِنْ أَصْحَٰبِ ٱلْيَمِينِ ﴿٩٠﴾ فَسَلَٰمٌ لَّكَ مِنْ أَصْحَٰبِ ٱلْيَمِينِ ﴿٩١﴾ وَأَمَّآ إِن كَانَ
مِنَ ٱلْمُكَذِّبِينَ ٱلضَّآلِّينَ ﴿٩٢﴾ فَنُزُلٌ مِّنْ حَمِيمٍ ﴿٩٣﴾ وَتَصْلِيَةُ جَحِيمٍ ﴿٩٤﴾
إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ حَقُّ ٱلْيَقِينِ ﴿٩٥﴾ فَسَبِّحْ بِٱسْمِ رَبِّكَ ٱلْعَظِيمِ ﴿٩٦﴾

57 سُورَةُ الحَدِيدِ مَدَنِيَّة
وَهِيَ ثَمَانٍ وَعِشْرُونَ ءَايَة 28

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

سَبَّحَ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿١﴾
لَهُۥ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ يُحْيِۦ وَيُمِيتُ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ﴿٢﴾
هُوَ ٱلْأَوَّلُ وَٱلْءَاخِرُ وَٱلظَّٰهِرُ وَٱلْبَاطِنُ وَهُوَ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمٌ ﴿٣﴾

80. Haƙiƙa shi abin karantawan nan a gareku, lallai alƙur'anine mai girma.
81. A cikin abin mbutuwa, abin boyewa (Shine mus'hafi abin kiyayewa daga canjawa da mu-sanyawa).
82. Ba mai shafarsa sai masu tsarki, (waɗanda suka tsarkake kawu-kansu daga karrai).
83. Saukarwa ne daga Ubangijin ta-likai.
84. Shin to da wannan alƙur'ani ku kuke wulaƙantawa?
85. Kuke sanya godiyar arzikinku (wato ruwa,) cewa ku kuna ƙaryata ƙaryatawa (da shayarwar Allah, saboda cewarku an shayar da mu da tauraro kaza).
86. To me yasa lokacin da rai tazo makogaro, (wato matafiyar abinci).
87. Alhali ku ya mahalartan ma-tacce, kuna dubansa.
88. Alhali mune mafi kusa daga gareshi (da iliminmu), amma baku fahimci hakan ba.
89. Me ya sa inkun kasance ba aba-ban yiwa sakamako ba (wato baza a tashe ku a rayar daku, ba?).
90. Ku komo dan ran (izuwa jiki bayan tazo maƙogwaro) inkun kasance magasgata, (a cikin abinda kuka riya).
91. To amma in mataccen ya ka-sance daga ababan kusantawa.
92. To hutawa da arziki mai kyau, da aljannar ni'ima (sun tabbata a gareshi.)
93. Amma in ya kasance daga ma'abota dama.
94. To kubuta daga azabata tabbata gareka (ya kai na cikin mutanen dama).
95. Amma in ya kasance daga mu-tane masu ƙaryatawa batattu.
96. To garar baƙi ta ruwan zafi (na gareshi).
97. Kuma shiga Jahannama (ya tab-bata a gareshi).
98. Haƙiƙa wannan shiga wuta to al-janna lallai Shine gaskiyar sa-kankancewa.
99. To sai ka tsarkake sunan Ubangijinka mai girma.

Wannan Sura Itace ce Suratul Hadidi

ayoyinta Ishirin da takwas (28)

Ta sauka bayan Suratul Zalzala Ina fara karatu dasunan ubangiji mai jinƙan mummai da kafirai a du-niya baki ɗaya, mai jinƙan muminai a lahira a keɓe.

(Wannan sura ta Kunshi tasbihi ga Allah, sannan neman imani, sannan ciyarwa fisabilillahi, sannan sakamakon imani da ciyarwa fi-sabilillahi ga ranar alƙiyama, sannan wa'azi ga mu-minai maza da mata. sannan bnyanm duniya da haƙiƙarta, sannan ginshiKan hukunce - hukunce, sannan sanya misali da Annabawa da al'umominsu. Ga ba ɗaya dai ita wannan sura tana kwadaitarwa a kan ciyarwa fi sabilillahi.)

(TASBIHI GA ALLAH SHI KADAI)

1. Abinda yake cikin sammai da ƙassaiya tsarkake Ubangijinsa da (harshen magana da 'harshen hali). Shine mabuwayi (cikin mulkinsa,) gwani a (cikin aikin-sa.)
2. Mulkin sammai da ƙassai yana gareshi, yana rayawa yana matarwa, (bayan ya raya,) shi mai ikone shi bisa kome.
3. Shine na farko (gaban kowane abu, bada faruwa ba,) Shine na Karshe (bayan kowane abu bada ƙurewa ba,) Shine mabayya-ni (da dalilai a kan samuwarsa,) Shine boyayye (ga buran mskar idanduna da sauran gabubuwan riska, hanci, kunne, hannu, harshe). Shi masanine da kome,

هُوَ ٱلَّذِے خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ فِے سِتَّةِ أَيَّامٖ ثُمَّ ٱسْتَوَىٰ عَلَى ٱلْعَرْشِ
يَعْلَمُ مَا يَلِجُ فِے ٱلْأَرْضِ وَمَا يَخْرُجُ مِنْهَا وَمَا يَنزِلُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ وَمَا يَعْرُجُ
فِيهَا وَهُوَ مَعَكُمُۥٓ أَيْنَ مَا كُنتُمْ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٞ (4) لَّهُۥ مُلْكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَإِلَى ٱللَّهِ تَرْجِعُ ٱلْأُمُورُ (5) يُولِجُ ٱلَّيْلَ فِے ٱلنَّهَارِ
وَيُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِے ٱلَّيْلِ وَهُوَ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ (6) * ءَامِنُواْ بِٱللَّهِ ثمن
وَرَسُولِهِۦ وَأَنفِقُواْ مِمَّا جَعَلَكُم مُّسْتَخْلَفِينَ فِيهِ فَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
مِنكُمْ وَأَنفَقُواْ لَهُمْ أَجْرٞ كَبِيرٞ (7) وَمَا لَكُمْ لَا تُومِنُونَ بِٱللَّهِ
وَٱلرَّسُولُ يَدْعُوكُمْ لِتُومِنُواْ بِرَبِّكُمْ وَقَدْ أَخَذَ مِيثَٰقَكُمْ إِن كُنتُم
مُّومِنِينَ (8) هُوَ ٱلَّذِے يُنَزِّلُ عَلَىٰ عَبْدِهِۦٓ ءَايَٰتِۢ بَيِّنَٰتٖ لِّيُخْرِجَكُم
مِّنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ وَإِنَّ ٱللَّهَ بِكُمْ لَرَءُوفٞ رَّحِيمٞ (9)
وَمَا لَكُمْ أَلَّا تُنفِقُواْ فِے سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلِلَّهِ مِيرَٰثُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ
لَا يَسْتَوِے مِنكُم مَّنْ أَنفَقَ مِن قَبْلِ ٱلْفَتْحِ وَقَٰتَلَ أُوْلَٰٓئِكَ أَعْظَمُ
دَرَجَةٗ مِّنَ ٱلَّذِينَ أَنفَقُواْ مِنۢ بَعْدُ وَقَٰتَلُواْ وَكُلّٗا وَعَدَ ٱللَّهُ
ٱلْحُسْنَىٰ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٞ (10) مَّن ذَا ٱلَّذِے يُقْرِضُ ٱللَّهَ
قَرْضًا حَسَنٗا فَيُضَٰعِفُهُۥ لَهُۥ وَلَهُۥٓ أَجْرٞ كَرِيمٞ (11)

4. Shine wanda ya halicci sammai da ƙassai a cikin miladarin kwana shida (da kwanakin duniya na farkonta Lahadi, na ƙarshenta Juma'a,) sannan ya daidaita kan karagar mulki (daidaituwa data dace dashi,) Yasan abinda yake shiga cikin ƙassai (kamar ruwa da matattu,) da abinda yake fitowa daga gareta (kamar tsirrai da baramu) da abinda yake sauka daga sama (kamar rahama da azaba) da abinda yake hawa cikinta (kamar ayyuka nagari da munana, hakana jirgin sama da makamantansa) shi yana taredaku ,(da iliminsa) inda duk kuka kasance. Allah masanine da abinda kuke aikatawa.
5. Mulkin sammai da ƙassai yana ga Allah (watau sarautarsu.) Izuwa ga Allah dukkan samammu suke komawa baki ɗayansu.
6. Yana shigar da dare cikin wuni, (sai wuni ya ƙaru dare ya ragu,) yana shigar da wuni cikin dare (sai dare ya ƙaru, wuni ya ragu,) masanine shi da haluluwan zukatan bayi (watau asirinta da ƙudure-ƙudurenta.)

(KWADAITARWA BISA IMANI DA CIYARWA FI SABILILLAHI)

7. Ku dauwama ga imani bisa ga Allah da ma'aikinsa (Sallallahu alaihi wa sallama) ku ciyar cikin inganta sha'anin Allah daga abinda yasanya ku wakilansa a cikinsa na dukiyar waɗanda suke gabanku, (da sannu na baya daku ,zasu mayeku a cikinsa. Ubangiji ya saukar da faɗinsa a cikin yaƙin Tabuka,)to waɗannan da suka bada gaskiya daga cikinku, suka ciyar (ishara ne izuwa ga Sayyadina Usmanu Raliyallahu Anhu), lada mai girma yana garesu.
8. Saboda Menene bazaku bada gaskiyaba da Allah (Yaku waɗannan kafirai?) ga ko manzon Allah yana kiranku donku bada gaskiya da Ubangijinku,alhali Allah ya karɓi alƙawarinku (tun Alamilzarri lokacin daya shaidad dasu bisa kawukansu,shin banine Ubangijinku bane? Sukace "kaine,)" inkun kasance masu nufin imani da Allah (to KUyi mazamaza ku bada gaskiya dashi.)
9. Shine wanda yake saukar da ayoyi mabaiyana bisa bawansa (ayoyin alƙur'ani) don yafish-sheku daga duffan kafirci izuwa hasken imani. Haƙiƙa, Ubangiji mai yawan jinƙaine gareku, mai rahama, (daya fish-sheku daga kafirci izuwa imani.)
10. Meke gareku cewa bazaku ciyar cikin inganta addinin Allah ba? Amma gadon sammai da ƙassai naga Allah (da abin da yake cikinsu, sai dukiyoyinku sun koma ga Allah bada ladan ciyarwa ba, saɓanin ciyarwarda za a baku ladan a kanta.) Wanda ya ciyar daga cikinku gaban buɗin Makkak bazai daidai da wanda baiyi ba, ! wadancananku sune mafi girman daraja daga waɗanda suka ciyar bayan buɗin Makkah!sukayi yaƙi, kowane ɗàya daga garesu Allah yayi musu alƙawarin aljanna. Allah masanine da abinda kuke aikatawa (zaiyi muku sakamako dashi.)
11. Wanene zai rantawa Allah rance kyakkyawa? (Shine ya ciyar da dukiyarsa a cikin inganta addinin Allah.) Ubangiji ya ninninka masa sakamako a gareshi, lada mai girma yana gareshi (tareda ninkawannan.)

يَوْمَ تَرَى ٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ يَسْعَىٰ نُورُهُم بَيْنَ أَيْدِيهِمْ وَبِأَيْمَٰنِهِم
بُشْرَىٰكُمُ ٱلْيَوْمَ جَنَّٰتٌ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا
ذَٰلِكَ هُوَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿12﴾ يَوْمَ يَقُولُ ٱلْمُنَٰفِقُونَ وَٱلْمُنَٰفِقَٰتُ
لِلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱنظُرُونَا نَقْتَبِسْ مِن نُّورِكُمْ قِيلَ ٱرْجِعُوا۟ وَرَآءَكُمْ
فَٱلْتَمِسُوا۟ نُورًا فَضُرِبَ بَيْنَهُم بِسُورٍ لَّهُۥ بَابٌۢ بَاطِنُهُۥ فِيهِ ٱلرَّحْمَةُ
وَظَٰهِرُهُۥ مِن قِبَلِهِ ٱلْعَذَابُ ﴿13﴾ يُنَادُونَهُمْ أَلَمْ نَكُن مَّعَكُمْ قَالُوا۟ بَلَىٰ وَلَٰكِنَّكُمْ
فَتَنتُمْ أَنفُسَكُمْ وَتَرَبَّصْتُمْ وَٱرْتَبْتُمْ وَغَرَّتْكُمُ ٱلْأَمَانِىُّ حَتَّىٰ
جَآءَ أَمْرُ ٱللَّهِ وَغَرَّكُم بِٱللَّهِ ٱلْغَرُورُ ﴿13﴾ فَٱلْيَوْمَ لَا يُؤْخَذُ مِنكُمْ
فِدْيَةٌ وَلَا مِنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مَأْوَىٰكُمُ ٱلنَّارُ هِىَ مَوْلَىٰكُمْ وَبِئْسَ ٱلْمَصِيرُ ﴿14﴾
* أَلَمْ يَأْنِ لِلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَن تَخْشَعَ قُلُوبُهُمْ لِذِكْرِ ٱللَّهِ ربع
وَمَا نَزَلَ مِنَ ٱلْحَقِّ وَلَا يَكُونُوا۟ كَٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ
مِن قَبْلُ فَطَالَ عَلَيْهِمُ ٱلْأَمَدُ فَقَسَتْ قُلُوبُهُمْ وَكَثِيرٌ مِّنْهُمْ
فَٰسِقُونَ ﴿15﴾ ٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ يُحْىِ ٱلْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَا
قَدْ بَيَّنَّا لَكُمُ ٱلْءَايَٰتِ لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿16﴾ إِنَّ ٱلْمُصَّدِّقِينَ وَٱلْمُصَّدِّقَٰتِ
وَأَقْرَضُوا۟ ٱللَّهَ قَرْضًا حَسَنًا يُضَٰعَفُ لَهُمْ وَلَهُمْ أَجْرٌ كَرِيمٌ ﴿17﴾

12. (Ambaci) ranar da kake ganin muminai maza da mata hasken suna tafe tsakanin hannayansu wato gabansu, hakanan da damammakinsu (anace dasu:) "albishirinku wannan rana, al jannatai (ku shige ta,) ƙoramu suna gudana ƙarƙashin ta masu dauwama a cikinta, wancananka shine rabo mai girma."

(MUNAFUkAI RANAR ALƘIYAMA)

13 Ranar da munafukai maza da mata suke faɗà ga waɗànda suka bada gaskiya, "Mu ɗosana daga haskenku," sai ace da su (don izgili dasu,) "ku koma bayanku, ku nemi haske," (suka koma,) sai akayi datsiya a tsakanin muminai da katanga, (Itace katangar La'arafu,) yana da kyaur, cikinsa akwai rahama, daga jihar muminai,) bayansa (daga jihar munafukai) azaba tana daga garesu, suna kiransu, shin bamu kasance tareda ku bane a kan ɗà'a? sai suce: "kun kasance taredamu, saidai ku kun futunci kawukanku (da munafunci,) kunyi sauraron masifun zamani daga garemu, kunyi kokonto cikin addinin Musulunci, gurace-gurace sun ruɗèku har mutuwa tazo, mai ruɗi da Allah Shaiɗàn shine ya ruɗeku.

14. To a yau baza a karɓi jiziya daga gareku ba, wato fansa, wala daga waɗànda suka kafirta, wutace makomarku Itace tafi dacewa daku, tur makoma ita!

(WA'AZI DA SHIRYARWA)

15. Shin bai yanzunta ba ga waɗànda suka bada gaskiya (ta sauka a cikin Sahabbai yardar ! Allah ta tabbata a garesu yayin ! da suka yawaita kakaci) zukatansu su sunkuya ga anbàton Allah da abinda ya sauka na daga Alƙur'ani bazasu kasance kamar waɗanda kabasu littafi ba -tun gaba (sune Yahudu da Nasara.) Zamani ya tsawaita garesu (tsakaninsu da Annabawansu tun gabansu zukatansu suka ! ƙeƙashe, (basuyi taushi da anbaton Allah ba,) yawanci daga cikinsu fasiƙai ne.

16. Ku sani (yaku muminai ababan !. anbato,) haƙiƙa Ubangiji yana raya ƙasa (da tsiri) bayan ta ƙeƙashe, (hakanan yake aikatawa ga zukatanku, da maida ita izuwa khushu'i, wato ƙanƙan dakai da zikirullahi) donku hankalta.

17. Haƙiƙa masu yin sadaka maza da mata, kuma suka rantawa Allah rance kyakkyawa, ana nin ninka musu sakamakon rancensu, lada mai girma na garesu.

وَالذِينَ ءَامَنُواْ بِاللَّهِ وَرُسُلِهِۦٓ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ الصِّدِّيقُونَ
وَالشُّهَدَآءُ عِندَ رَبِّهِمْ لَهُمْ أَجْرُهُمْ وَنُورُهُمْ وَالذِينَ كَفَرُواْ
وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ الْجَحِيمِ (18) اِعْلَمُوٓاْ أَنَّمَا الْحَيَوٰةُ
الدُّنْيَا لَعِبٌ وَلَهْوٌ وَزِينَةٌ وَتَفَاخُرُۢ بَيْنَكُمْ وَتَكَاثُرٌ فِے الْأَمْوَٰلِ
وَالْأَوْلَٰدِ كَمَثَلِ غَيْثٍ أَعْجَبَ الْكُفَّارَ نَبَاتُهُۥ ثُمَّ يَهِيجُ فَتَرَىٰهُ
مُصْفَرّاً ثُمَّ يَكُونُ حُطَٰماً وَفِے الْأٓخِرَةِ عَذَابٌ شَدِيدٌ
وَمَغْفِرَةٌ مِّنَ اللَّهِ وَرِضْوَٰنٌ وَمَا الْحَيَوٰةُ الدُّنْيَآ إِلَّا مَتَٰعُ
الْغُرُورِ (19) سَابِقُوٓاْ إِلَىٰ مَغْفِرَةٍ مِّن رَّبِّكُمْ وَجَنَّةٍ عَرْضُهَا
كَعَرْضِ السَّمَآءِ وَالْأَرْضِ أُعِدَّتْ لِلذِينَ ءَامَنُواْ بِاللَّهِ وَرُسُلِهِۦ
ذَٰلِكَ فَضْلُ اللَّهِ يُوتِيهِ مَن يَّشَآءُ وَاللَّهُ ذُو الْفَضْلِ الْعَظِيمِ (20)
* مَآ أَصَابَ مِن مُّصِيبَةٍ فِے الْأَرْضِ وَلَا فِےٓ أَنفُسِكُمْ إِلَّا فِے كِتَٰبٍ
مِّن قَبْلِ أَن نَّبْرَأَهَآ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى اللَّهِ يَسِيرٌ (21) لِّكَيْلَا تَأْسَوْاْ
عَلَىٰ مَا فَاتَكُمْ وَلَا تَفْرَحُواْ بِمَآ ءَاتَىٰكُمْ وَاللَّهُ لَا يُحِبُّ
كُلَّ مُخْتَالٍ فَخُورٍ (22) الذِينَ يَبْخَلُونَ وَيَأْمُرُونَ النَّاسَ
بِالْبُخْلِ وَمَن يَتَوَلَّ فَإِنَّ اللَّهَ الْغَنِيُّ الْحَمِيدُ (23)

ثمن

18. Waɗanda suka bada gaskiya da Allah da manzanninsa waɗàncananka sune haƙiƙa sadaukai, (wato masu isa matuka a cikin ban gaskiya,) to Shahidai kuwa ladansu yana garesu da haskensu, waɗànda suka kafirta, suka ƙaryata ayoyinmu, waɗancananka sune'yan wuta.

(HAƘIƘAR DUNIYA DA LAHIRA)

19. Kusani dahir dai rayuwar duniya wasane da shagala da ƙelƙelin-banza da fariya tsakaninku da yawaitawa a cikin tara dukiyoyi da 'ya'yaye, (amma ɗa'o'i da abinda yake taimako a kanta to wannan yana daga al'amuran lahira, ita duniya a cikin baku sha'awa da sheƙewarta) kamar misalin ruwane da tsirinsa ya baiwa manoma mamaki, sannan ya ƙeƙashe ka ganshi a yanƙwane, sannan ya zama tarkace, (iska ta sheƙeshi.) Azaba mai tsanani ta tabbata a lahira ga wanda ya fifita duniya a kanta,) da gafara ' daga Allah da yarda (ga wanda bai fifita duniya a kan lahira ba,) rayuwar duniya bata kashe ba (a cikin moriyarta,) sai anfanin ruɗi.

20. Kuyi gaggawa izuwa gafara daga Ubangijinku, da aljanna wacce faɗinta kamar faɗin sammai da ƙassai, (da za a sada ɗàyarsu ga ɗàyar,) an tanadeta ga waɗànda suka bada gaskiya da Allah da ma'aikinsa, wanɗancananka falalar Allah ne, yana bashcshi ga wanda yaga dama, Ubangiji ma'abocin falala ne mai girma.

(AL'AMARI DUKKANSA NA ALLAH NE)

21. Babu wani abu da zai samu mummuni na musiba a cikin ƙasa kamar fari, wala a cikin kawukanku (kamar rashin lafiya da rashin ɗa) face yana cikin littafi (na Lauhul Mahafuzu,) tun gaban bamu halicceta ba, (hakanan ma ni'imar,) haƙiƙa wancanenka mai sauƙi ne bisa Allah (Ubangiji ya bada labari bisa wannan.)

22. Don kada kuyi baƙin ciki bisa abinda ya tsene muku kuyi farin ciki (na fariya) da abinda yabaku (sai dai farin ciki na godiya.) Ubangiji baya son mai fariya a kan mutane.

23. Duk waɗànda suke rowa (da abinda ya wajaba a kansu) suke umarnin mutane da suyi rowa (dashi, azaba mai raɗaɗi ta tabbata garesu,) wanda ya bada baya (ga buran abinda ya wajaba a kansa,) to haƙiƙa Ubangiji shine mawadaci (ga buran Waninsa,) abin godewa (ga waliyansa.)

لَقَدْ أَرْسَلْنَا رُسُلَنَا بِالْبَيِّنَٰتِ وَأَنزَلْنَا مَعَهُمُ الْكِتَٰبَ وَالْمِيزَانَ
لِيَقُومَ النَّاسُ بِالْقِسْطِ وَأَنزَلْنَا الْحَدِيدَ فِيهِ بَأْسٌ شَدِيدٌ
وَمَنَٰفِعُ لِلنَّاسِ وَلِيَعْلَمَ اللَّهُ مَن يَنصُرُهُۥ وَرُسُلَهُۥ بِالْغَيْبِ
إِنَّ اللَّهَ قَوِيٌّ عَزِيزٌ ﴿24﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا نُوحًا وَإِبْرَٰهِيمَ وَجَعَلْنَا
فِي ذُرِّيَّتِهِمَا النُّبُوٓءَةَ وَالْكِتَٰبَ فَمِنْهُم مُّهْتَدٍ وَكَثِيرٌ مِّنْهُمْ
فَٰسِقُونَ ﴿25﴾ ثُمَّ قَفَّيْنَا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم بِرُسُلِنَا وَقَفَّيْنَا بِعِيسَى
ابْنِ مَرْيَمَ وَءَاتَيْنَٰهُ الْإِنجِيلَ وَجَعَلْنَا فِي قُلُوبِ الَّذِينَ اتَّبَعُوهُ
رَأْفَةً وَرَحْمَةً وَرَهْبَانِيَّةً ابْتَدَعُوهَا مَا كَتَبْنَٰهَا عَلَيْهِمْ
إِلَّا ابْتِغَآءَ رِضْوَٰنِ اللَّهِ فَمَا رَعَوْهَا حَقَّ رِعَايَتِهَا
فَـَٔاتَيْنَا الَّذِينَ ءَامَنُوا مِنْهُمْ أَجْرَهُمْ وَكَثِيرٌ مِّنْهُمْ فَٰسِقُونَ ﴿26﴾
يَٰٓأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُوا اتَّقُوا اللَّهَ وَءَامِنُوا بِرَسُولِهِۦ يُؤْتِكُمْ
كِفْلَيْنِ مِن رَّحْمَتِهِۦ وَيَجْعَل لَّكُمْ نُورًا تَمْشُونَ بِهِۦ وَيَغْفِرْ لَكُمْ
وَاللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿27﴾ لِئَلَّا يَعْلَمَ أَهْلُ الْكِتَٰبِ
أَلَّا يَقْدِرُونَ عَلَىٰ شَيْءٍ مِّن فَضْلِ اللَّهِ وَأَنَّ الْفَضْلَ
بِيَدِ اللَّهِ يُؤْتِيهِ مَن يَشَآءُ وَاللَّهُ ذُو الْفَضْلِ الْعَظِيمِ ﴿28﴾

(ASALAN HUKUNCE-HUKUNCE A CIKIN MUSULUNCI)

24. Haƙiƙa mun aiko jakadunmu Mala'iku izuwa Annabawa da hujjoji mabaiyana, mun saukarda littattafai taredasu da ma'auni don mutane su tsaya da adalci, haƙiƙa mun fitar da ƙarfe ! (wato mun fitar dashi daga baramu bayan mun saukar da Annabi Adamu daga Aljanna yana tareda abubuwa guda shida na baƙin ƙarfe, kamar maƙera da arautaki da guduma da alluna da zarto da masaba, an saukar da ƙarfe) donya taimaka a yaƙi ! kuma ya anfani mutane, kuma don Allah ya nuna wanda zai ! taimakeshi (wato zai taimaki addininsa da alolin yaƙi na baƙin ƙarfe kamar kansakali da ' waninsa da alƙalami wato mai taimako ga talifin malamai, wato su taimaki; Allah) batareda sun ganshi ganin ido ba, (wato sai ganin zuci.) Haƙiƙa Ubangiji mai ƙarfine mabuwayi ! (bashida buƙata izuwa taimako.)

(MAƘASUDI DAGA AIKO MANZANNI)

25 Haƙiƙa mun aiko Annabi Nuhu da Annabi Ibrahim, (tsira da aminci su tabbata a garesu,) mun sanya Annabci da littattafai huɗu(4)a cikin zuciyarsu akwai daga garesu mai shiriya, yawaici daga cikinsu fasiƙaine.

26. Sannan muka biyar a gurabansu da manzanninmu, muka biyar da Annabi Isa ɗan Maryama, muka bashi Injila, muka sanya tsananin jinƙai da rahama da sufantaka a cikin zukatan waɗanda suka bishi bamu umarcesu da ita ba, sai dai sun aikatata ne don neman yardar Allah to basu kiyayeta haƙiƙanin kiyayewa ba (don yawaici daga garesu sun barta, sun kafirce da addinin Isa, sun shiga addinin sarkinsu, yawaici daga garesu sun wanzu bisa addinin Annabi Isa, suka bada gaskiya da Annabinmu,) muka baiwa waɗanda suka bada gaskiya dashi sakamako, yawaici daga garesu fasiƙaine.

27. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya (da Annabi Isa!) kuji tsoron Allah ku bada gaskiya ga Manzonsa, ya baku rabo biyu daga rahamarsa, (saboda kun bada gaskiya da Annabawa guda biyu,) kuma zai sanya muku haske da zakuyi tafiya dashi (kan siraɗi) zaiyi gafara gareku, Allah mai gafarane mai jinƙai. wai daga garesu mai shiriya, ya waici daga cikinsu fasikai ne.

26. Sannan muka biyar a gurabansu da manzanninmu, muka biyar da Annabi Isa cfan Maryama, muka ba shi Injila, muka sanya tsananin jin kai da rahama da sufantaka a cikin zukatan wadanda suka bi shi ba mu umarce su da ita ha, sai dai sun aikata ta ne don neman yardar Allah to ba su kiyayeta hakikanin kiyayewa ha (don ya waici daga garesu sun bar ta, sun kafirce da addinin Isa, sun shiga addinin sarkinsu, yawaici daga garesu sun wanzu bisa ad dinin Annabi Isa, suka ba da gaskiya da Annabinmu,) muka bai wa wacfanda suka ha da gas kiya da shi sakamako, yawaici daga garesu fasikai ne.

27. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya (da Annabi Isa!) kuji tsoron Allah ku bada gaskiya ga Manzonsa, ya baku rabo biyu daga rahamarsa, (saboda kun bada gaskiya da Annabawa guda biyu,) kuma zai sanya muku haske da zakuyi tafiya dashi (kan siraɗi) zaiyi gafara gareku, Allah mai gafarane mai jinƙai.

28. (yasanar daku)don ma,abota littafi (na attaura wadanda basu bada gaskiyaba)su sani cewa su basu da iko bias komai na daga falalar Allah (sabanin abin da yake cikin zukatansu bisa riyawarsu ,cewa sum asana Allah ne)kuma cewa falalatana gurin Allah,ya basheta ga wanda yaga dama (ya baiwa muminailadansu sau biyu) ubangiji mai baiwa ne mai girma

سُورَةُ الْمُجَادِلَةِ مَدَنِيَّة 58
وَهِيَ ثِنْتَانِ وَعِشْرُونَ ءَايَة 22

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

حزب

* قَدْ سَمِعَ اللَّهُ قَوْلَ الَّتِي تُجَادِلُكَ فِي زَوْجِهَا وَتَشْتَكِي إِلَى اللَّهِ
وَاللَّهُ يَسْمَعُ تَحَاوُرَكُمَا إِنَّ اللَّهَ سَمِيعٌ بَصِيرٌ (1) الَّذِينَ يَظَّهَّرُونَ
مِنكُم مِّن نِّسَآئِهِم مَّا هُنَّ أُمَّهَاتِهِمْ إِنْ أُمَّهَاتُهُمُ إِلَّا اللَّاءِ وَلَدْنَهُمْ
وَإِنَّهُمْ لَيَقُولُونَ مُنكَرًا مِّنَ الْقَوْلِ وَزُورًا وَإِنَّ اللَّهَ لَعَفُوٌّ غَفُورٌ (2)
وَالَّذِينَ يَظَّهَّرُونَ مِن نِّسَآئِهِمْ ثُمَّ يَعُودُونَ لِمَا قَالُواْ فَتَحْرِيرُ رَقَبَةٍ
مِّن قَبْلِ أَن يَتَمَآسَّا ذَٰلِكُمْ تُوعَظُونَ بِهِۦ وَاللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ (3)
فَمَن لَّمْ يَجِدْ فَصِيَامُ شَهْرَيْنِ مُتَتَابِعَيْنِ مِن قَبْلِ أَن يَتَمَآسَّا
فَمَن لَّمْ يَسْتَطِعْ فَإِطْعَامُ سِتِّينَ مِسْكِينًا ذَٰلِكَ لِتُؤْمِنُواْ بِاللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَتِلْكَ
حُدُودُ اللَّهِ وَلِلْكَٰفِرِينَ عَذَابٌ أَلِيمٌ (4) إِنَّ الَّذِينَ يُحَآدُّونَ اللَّهَ وَرَسُولَهُۥ
كُبِتُواْ كَمَا كُبِتَ الَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ وَقَدْ أَنزَلْنَا ءَايَٰتٍ بَيِّنَٰتٍ وَلِلْكَٰفِرِينَ
عَذَابٌ مُّهِينٌ (5) يَوْمَ يَبْعَثُهُمُ اللَّهُ جَمِيعًا فَيُنَبِّئُهُم بِمَا عَمِلُواْ
أَحْصَىٰهُ اللَّهُ وَنَسُوهُ وَاللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ شَهِيدٌ (6)

Wannan Sura Itace Suratul Mijadalati
a Madina aka saukar da ita aya ishirin da ɗayace (21).
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan sura ta ƙunshi zihari da hukuncinsa sannan sakamakon wanda yake Mujadala da Allah sannan kuma magana kan ganawa da saɓo da shishshigi, sannan bayanin ladabin zamanta kaiya da anbaton munafukai da sakamakonsu, da hukuncin wanda ya riƙi kafirai ababan soyayya, ba muminaiba da bayanin ba'alin adabu da sha'anunuwan musulunci).

(ZIHARI DA HUKUNCINSA DA KAFFARARSA)

1. Haƙiƙa Ubangiji yaji maganar matannan da take komemeniyar magana a gareka (ya wannan Annabi Sallallahu alaihi wa sallama Itace Haulatu 'yar Sa'alabata) a cikin mijinta, (wanda yayi mata zihari wato ya bayantar da itada faɗinsa, ke a gare ni kamar bayan mahaifiyata kike, alhali ta tambayi manzon Allah Sallallahu alaihi wa sallama ga wancananka, ya amsa matada cewa, haƙiƙa ita ta haramta a gareshi, bisa dogaro kan abinda aka saɓa a garesu, shine cewa zihari wato bayantawa ya wajabta rabuwa ta (har abada,) take kai karan (kadaitattada talaucinta, alhali ga kananan yara waɗanda in ta tarasu izuwa gareshi su tozarta, in kuma izuwa gareshi su tozarta, in kuma izuwa gareta su yunwata,) alhali Allah yana jin asheshenîyar maganarku Ubangiji mai jine mai sani.
2. Waɗanda suke bayantar da matansu daga cikinku na matayansu, su matayan nan ba iyayen suneba, babu iyayensu sai waɗannan da suka haifesu, haƙiƙa su (saboda ziharin nan) suna faɗin mummuna ne na magana da ƙarya, haƙiƙa Ubangiji lallai mai afuwane mai gafara (ga wanda ya bayantar da matarsa da kaffara).
3. Waɗannan dasuke zihari na bayantawa ga matayensu, sannan su koma ga abinda suka faɗa (cikinsa, shine su saɓeshi, su riƙe wacce suka bayantar, wanda shine saɓanin ziharin abin nufi na daga kwatanta mace da haramci). To 'yanta wuyaye ne a kansu tun gaban basu shafi juna da taka ba, (wato saduwa), wancanenku anayi muku wa'azi dashi. Allah masanine da abinda kuke aikatawa.
4. To wanda bai sami wuyaye dazai yanta ba to azumin wata biyune ke kansa, majeranta guda biyu tun gaban basu sadu da juna ba, to duka wanda bai sami damar yin azumin wata biyu ba to ya ciyar da miskini sittin, (mudu ga kowane miskini, na daga marinjayin abincin gari,) wancananka (sauwakewa cikin kaffara) donku bada gaskiya da Allah da ma'aikinsa ne, wakancanenka (hukunce-hukunce ababan anbato,) iyakokin Allah ne, azaba mai raɗaɗi ta tabbata ga masu ƙaryatawa (da ita).

(ALLAH MAI KEWAYEWA NE DA KOMAI)

5. Haƙiƙa waɗannan dasuke kangarewa Allah da ma'aikinsa, an tursasasu tamfar daka tursasa waɗanda suke gabansu, (a cikin saɓawarsu ga manzanninsu,) haƙiƙa mun saukar da ayoyi mabaiyana, (masu shiryarwa bisa gaskiyar manzon,) azaba mai wulaƙantarwa ta tabbata ga masu wulaƙantar da ayoyin Allah.
6. A ranar da Allah yake tashinsu baki ɗaya ya basu labari da abinda suka aikata, Allah ya kewaye da saninsa suko sun mance shi Ubangiji mai kallon komaine.

أَلَمْ تَرَ أَنَّ اللَّهَ يَعْلَمُ مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ مَا يَكُونُ
مِن نَّجْوَىٰ ثَلَاثَةٍ إِلَّا هُوَ رَابِعُهُمْ وَلَا خَمْسَةٍ إِلَّا هُوَ سَادِسُهُمْ
وَلَا أَدْنَىٰ مِن ذَٰلِكَ وَلَا أَكْثَرَ إِلَّا هُوَ مَعَهُمْ أَيْنَ مَا كَانُوا
ثُمَّ يُنَبِّئُهُم بِمَا عَمِلُوا يَوْمَ الْقِيَامَةِ إِنَّ اللَّهَ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمٌ ﴿7﴾
* أَلَمْ تَرَ إِلَى الَّذِينَ نُهُوا عَنِ النَّجْوَىٰ ثُمَّ يَعُودُونَ لِمَا نُهُوا عَنْهُ ثمن
وَيَتَنَاجَوْنَ بِالْإِثْمِ وَالْعُدْوَانِ وَمَعْصِيَتِ الرَّسُولِ وَإِذَا جَاءُوكَ حَيَّوْكَ
بِمَا لَمْ يُحَيِّكَ بِهِ اللَّهُ وَيَقُولُونَ فِي أَنفُسِهِمْ لَوْلَا يُعَذِّبُنَا اللَّهُ بِمَا نَقُولُ
حَسْبُهُمْ جَهَنَّمُ يَصْلَوْنَهَا فَبِئْسَ الْمَصِيرُ ﴿8﴾ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ
آمَنُوا إِذَا تَنَاجَيْتُمْ فَلَا تَتَنَاجَوْا بِالْإِثْمِ وَالْعُدْوَانِ وَمَعْصِيَتِ
الرَّسُولِ وَتَنَاجَوْا بِالْبِرِّ وَالتَّقْوَىٰ وَاتَّقُوا اللَّهَ الَّذِي إِلَيْهِ
تُحْشَرُونَ ﴿9﴾ إِنَّمَا النَّجْوَىٰ مِنَ الشَّيْطَانِ لِيَحْزُنَ الَّذِينَ آمَنُوا
وَلَيْسَ بِضَارِّهِمْ شَيْئًا إِلَّا بِإِذْنِ اللَّهِ وَعَلَى اللَّهِ فَلْيَتَوَكَّلِ الْمُؤْمِنُونَ ﴿10﴾
يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا إِذَا قِيلَ لَكُمْ تَفَسَّحُوا فِي الْمَجْلِسِ فَافْسَحُوا
يَفْسَحِ اللَّهُ لَكُمْ وَإِذَا قِيلَ انشُزُوا فَانشُزُوا يَرْفَعِ اللَّهُ الَّذِينَ آمَنُوا مِنكُمْ
وَالَّذِينَ أُوتُوا الْعِلْمَ دَرَجَاتٍ وَاللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ ﴿11﴾

7. Shin bakasan ccwa Allah yasan abinda yake cikin sammai da ƙassai bane? Ba wata ganawa ta mutum uku face Ubangiji na huđunsune (da saninsa,) wala ganawar mutum biyar, face shi na shidansu ne, wala mafi ƙanƙanta daga wannan, wala mafi yawa, face shi yana taredasu duk inda suka kasance, sannan ya basu labarin abinda suka aikata ranar alƙiyama, haƙiƙa Ubangiji masanine da kowane abu.

(LADABAN GANAWA A CIKIN ADDININ MUSULUNCI)

8. Shin bakai duba ga wađanda aka hanasu ganawa da zunubi ba sannan suke komawa ga ɓuran abinda aka hanasu ga ɓuransa, suke gamawa da zunubi dashishshigi da saɓon Manzon Allah (Sallallahu alaihi wa sallama, sune Yahudu, Annabi ya hanesu ga ɓuran abinda suke aikatawa na ganawarsu a ɓoye, suna masu duba izuwa muminai donsu darsar da kokonto a cikin zukatan muminai) idan sunzo maka saisu gaisheka da abinda Allah bai gaisheka dashi ba, (shine fađinsu ASSAMU ALAIKA, wato mutuwa a kanka) suna fađi a cikin kawukansu me yasa Ubangiji baiyi mana azaba ba saboda abinda muke fađana daga gaisuwa (indashi annabi ne) Jahannama ta ishesu, zasu shigeta tur makoma ita!

9. Yaku wađanda kuka bada gaskiya, idan zaku gana kadaku ,gana da zunubi da shishshigi da saɓon manzo. Ku gana da bin Allah da tsoron Allah, kuji tsoron Allah wanda ake taraku izuwa gareshi.

10. Ganawa da zunibi da makamancinsa daga Shaiđan yake, (wato daga cusawarsa donya baƙantawa wađanda suka bada gaskiya,) shi bazai cucesu da komai ba saida izinin Allah, muminai su dogara bisa Allah shi kađai.

(WANI ABU NA LADABIN MUSULUNCI CIKIN ZAMA)

11. Yaku wađanda kuka bada gaskiya! in Ance ku yalwata a majalisar Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama) to ku yalwata, (har wanda yazo daga baya ya zauna,) Allah ya yawaita muku (aljanna,) in Ance ku tashi (izuwa salla da waninta na aikin alheri,) to ku tashi. Allah ya đaukaka wađanda suka bada gaskiya sukayi aikin alheri da wanin wannan Allah ya đaukaka wađanda aka basu ilimi da darajoji a aljanna, Ubangiji masanine da abinda kuke aikatawa.

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا نَٰجَيۡتُمُ ٱلرَّسُولَ فَقَدِّمُواْ بَيۡنَ يَدَيۡ نَجۡوَىٰكُمۡ صَدَقَةٗۚ
ذَٰلِكَ خَيۡرٞ لَّكُمۡ وَأَطۡهَرُۚ فَإِن لَّمۡ تَجِدُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٌ ﴿12﴾
ءَأَشۡفَقۡتُمۡ أَن تُقَدِّمُواْ بَيۡنَ يَدَيۡ نَجۡوَىٰكُمۡ صَدَقَٰتٖۚ فَإِذۡ لَمۡ تَفۡعَلُواْ وَتَابَ ٱللَّهُ
عَلَيۡكُمۡ فَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُواْ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥۚ وَٱللَّهُ
خَبِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ ﴿13﴾ * أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ تَوَلَّوۡاْ قَوۡمًا غَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِم
مَّا هُم مِّنكُمۡ وَلَا مِنۡهُمۡ وَيَحۡلِفُونَ عَلَى ٱلۡكَذِبِ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ﴿14﴾
أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُمۡ عَذَابٗا شَدِيدًاۖ إِنَّهُمۡ سَآءَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ﴿15﴾
ٱتَّخَذُوٓاْ أَيۡمَٰنَهُمۡ جُنَّةٗ فَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ فَلَهُمۡ عَذَابٞ
مُّهِينٞ ﴿16﴾ لَّن تُغۡنِيَ عَنۡهُمۡ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُهُم مِّنَ ٱللَّهِ شَيۡـًٔاۚ
أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿17﴾ يَوۡمَ يَبۡعَثُهُمُ ٱللَّهُ
جَمِيعٗا فَيَحۡلِفُونَ لَهُۥ كَمَا يَحۡلِفُونَ لَكُمۡ وَيَحۡسَبُونَ أَنَّهُمۡ عَلَىٰ شَيۡءٍۚ
أَلَآ إِنَّهُمۡ هُمُ ٱلۡكَٰذِبُونَ ﴿18﴾ ٱسۡتَحۡوَذَ عَلَيۡهِمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ
فَأَنسَىٰهُمۡ ذِكۡرَ ٱللَّهِۚ أُوْلَٰٓئِكَ حِزۡبُ ٱلشَّيۡطَٰنِۚ أَلَآ إِنَّ حِزۡبَ ٱلشَّيۡطَٰنِ
هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ﴿19﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ يُحَآدُّونَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓ أُوْلَٰٓئِكَ
فِي ٱلۡأَذَلِّينَ ﴿20﴾ كَتَبَ ٱللَّهُ لَأَغۡلِبَنَّ أَنَا۠ وَرُسُلِيٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ قَوِيٌّ عَزِيزٞ ﴿21﴾

رُبع

(GANAWA DA MA'AIKIN ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAMA)

12. Yaku wadanda kuka bada gaskiya! in zaku gana da ma'aikin Allah (Sallallahu alaihi wa sallama) to ku gabatar da sadaka gaban ganawarku, wancananka shine yafi alheri kuma yafi tsarkakewa ga zunubanku, idan baku sami abinda zakuyi sadaka dashi 'ba, to hakika Ubangiji mai gafara ne mai jinkai (wato ba laifi gareku a cikin ganawa ba tareda sadaka ba, sannan aka shafe wannan da fadinsa.)
13. Shin kunji tsoron (talauci ne) daga gabatarwar sadakoki a gaban ganawarku? tunda baku aikata wannan sadaka ba Allah yakomo daku ,ga buranta (wato ga buran wajabcinta,) to ku tsaida salla ku bada zakka ku dauwama a kan bin Allah da ma'aikinsa, Ubangiji masanine da abinda kuke aikatawa(Hadakai Da Wadansu Muminai)
14. Baka duba bane izuwa wadannan munafikai da suka jibinci mutane (Yahudu) da Allah yayi azaba garesu su (munafukai) basa cikinsu (Yahuduwa, wato su 'yan muzabzabai ne wato 'yan tawaiwai ne,) suna rantsuwa kan karya wato fadinsu cewa su muminai ne alhali su sunsan cewa su makaryata ne (cikinsa).
15. Allah ya tanadi azaba mai tsanani a garesu, hakika su abinda suke aikatawa (na sabanni) ya mugusta.
16. Sun riki rantse-rantsensu garkuwa (a kan kawukansu da dukiyarsu, wato suttura,).Suka datse muminai da ita gaburan hanyar Allah, (wato yaki a cikinsu da kashe su da karbar dukiyarsu,) to azaba mai (wulakantarwa ta tabbata a garesu).
17. Dukiyoyinsu da 'ya'yansu basu wadatar dasu komai ga buran Allah ba, wadancanenka sune'yan wuta, su masu dauwama ne a cikinta.
18.Ambaci ranar da Allah yake tarasu baki daya, su rantse gareshi cewa su muminai ne tamfar dasuke rantsuwa gareku, suna zaton hakika cewa su suna kan wani abu (na daga anfanin rantsuwarsu ranar lahira, tamfar da sukayi anfani da ita a duniya) na'am, hakika su, sune ainahin makaryata.
19. Shaidan yayi zara dasu, (saboda da'arsu gareshi,) sai ya mantar dasu anbaton Allah wadancanenku sune rundunar shaidan,'e', hakika rundunar shaidan sune kadai tababbu.
20. Hakika wadanda suke kangarewa Allah da Ma'aikinsa, wadancanenka suna cikin kayayyu, Ubangiji ya hukunta a Lauhu Mahfuzu, Wallahi nine mai rinjaye nida jakaduna (da hujja ko kansakali,) hakika Ubangiji kakkarfa ne mabuwayi.
21. Baka samun mutane da suka bada gaskiya da Allah da ranar lahira suna dasawa da wanda ya kangarewa Allah,

لَا تَجِدُ قَوْماً يُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ وَالْيَوْمِ الْآخِرِ يُوَادُّونَ مَنْ حَادَّ اللَّهَ وَرَسُولَهُ
وَلَوْ كَانُوا آبَاءَهُمْ أَوْ أَبْنَاءَهُمْ أَوْ إِخْوَانَهُمْ أَوْ عَشِيرَتَهُمْ
أُولَٰئِكَ كَتَبَ فِي قُلُوبِهِمُ الْإِيمَانَ وَأَيَّدَهُم بِرُوحٍ مِّنْهُ وَيُدْخِلُهُمْ
جَنَّاتٍ تَجْرِي مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَارُ خَالِدِينَ فِيهَا رَضِيَ اللَّهُ عَنْهُمْ
وَرَضُوا عَنْهُ أُولَٰئِكَ حِزْبُ اللَّهِ أَلَا إِنَّ حِزْبَ اللَّهِ هُمُ الْمُفْلِحُونَ ﴿22﴾

59 سُورَةُ الحَشْرِ مَدَنِيَّةٌ
وَهِيَ أَرْبَعٌ وَعِشْرُونَ آيَةً 24

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

* سَبَّحَ لِلَّهِ مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ وَهُوَ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ ﴿1﴾ [ثمن]
هُوَ الَّذِي أَخْرَجَ الَّذِينَ كَفَرُوا مِنْ أَهْلِ الْكِتَابِ مِن دِيَارِهِمْ
لِأَوَّلِ الْحَشْرِ مَا ظَنَنتُمْ أَن يَخْرُجُوا وَظَنُّوا أَنَّهُم مَّانِعَتُهُمْ حُصُونُهُم
مِّنَ اللَّهِ فَأَتَاهُمُ اللَّهُ مِنْ حَيْثُ لَمْ يَحْتَسِبُوا وَقَذَفَ فِي قُلُوبِهِمُ
الرُّعْبَ يُخْرِبُونَ بُيُوتَهُم بِأَيْدِيهِمْ وَأَيْدِي الْمُؤْمِنِينَ
فَاعْتَبِرُوا يَا أُولِي الْأَبْصَارِ ﴿2﴾ وَلَوْلَا أَن كَتَبَ اللَّهُ عَلَيْهِمُ
الْجَلَاءَ لَعَذَّبَهُمْ فِي الدُّنْيَا وَلَهُمْ فِي الْآخِرَةِ عَذَابُ النَّارِ ﴿3﴾

22. koda makangaran nan sun kasance iyayensu (muminai) ko 'ya'yansu ko 'yan uwansu, ko danginsu, (Kai yaƙarsu zasuyi a kan imani, tamkar daya afku ga jama'a na Sahabbai; Allah ya ƙara musu yarda) wadancanenka (waɗanda basada sheseniya) Allah ya rubuta imani cikin zuciyarsu, ya ƙarfafesu da haske daga gareshi, kuma zai shigar dasu aljannatai, wacce ƙoramai suke gudana ƙarƙashinta, masu dauwama a cikinta, Allah ya yarda garesu sun yarda a gareshi (Shida ɗa'arsa, su kuma da sakamakonsa) wadancanenka sune rundunar Allah, (suna bin umarninsa, suna nisantar haninsa) lallai haƙiƙa rundunar Allah sune kaɗai masu rabauta.

Wannan Sura Itace Suratul Hashari

A Madina aka saukar da ita. Aya ishirin da hudu ce (24)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai ji Kan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan Sura ta ƙunshi ƙaurar da Baninnadiri da Hukuncin Fai'i a cikin Musulunci da matsayin Munafikai na Baninnairi, da Wa'azantar Musulmi da tsoron Allah da zance kan Alƙur'ani da gama sura da anbaton sunan Allah kyawawa).

(ƘAURATAR DA BANINNADIRI)

1. Abinda yake cikin sammai da ƙassai ya tsarkake Ubangiji shine mabuwayi, mai hikima (cikin mulkinsa da aikinsa).
2. Shine wanda yafitar da waɗanda suka kafirta daga mazowa littafi(Naliru), daga Yahudawa daga gidajensu izuwa farkon tarawa, (izuwa Sham, na ƙarshensa kuma, Saiyidina Umaru ya ƙauratar dasu a cikin Hilafatasa daga Aziri'atu izuwa Khaibara, bakuyi zato ba (ku muminai cewa sa fita ba,) zaton cewa su biranensu zata tsaresu daga azabar Allah, al'amarin Ubangiji yazo musu ta inda basu zata ba, (daga jihar muminai) Ubangiji ya jefa razani a cikin zukatansu (saboda kashe shugabansu Ka'abu ɗan Lasharafu) suna rusa dakunansu, (donsu cire abinda suka ga kyansa na azara da waninsa) da hannuwansu da hannuwan muminai, sai kuyi izna ya ma'abota hankula.
3. Badon Ubangiji ya rubuta ƙaura daga mazauninsu a kansu bada yayi musu azaba a duniya, azaba ta wuta ta tabbata garesu a lahira.

ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ شَآقُّواْ اُ۬للَّهَ وَرَسُولَهُۥۖ وَمَنْ يُّشَآقِّ اِ۬للَّهَ فَإِنَّ اَ۬للَّهَ
شَدِيدُ اُ۬لْعِقَابِۖ ﴿4﴾ مَا قَطَعْتُم مِّن لِّينَةٍ اَوْ تَرَكْتُمُوهَا قَآئِمَةً
عَلَىٰٓ أُصُولِهَا فَبِإِذْنِ اِ۬للَّهِ وَلِيُخْزِيَ اَ۬لْفَٰسِقِينَۖ ﴿5﴾ وَمَآ أَفَآءَ اَ۬للَّهُ
عَلَىٰ رَسُولِهِۦ مِنْهُمْ فَمَآ أَوْجَفْتُمْ عَلَيْهِ مِنْ خَيْلٍ وَلَا رِكَابٍۖ
وَلَٰكِنَّ اَ۬للَّهَ يُسَلِّطُ رُسُلَهُۥ عَلَىٰ مَنْ يَّشَآءُۖ وَاللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ
قَدِيرٌۖ ﴿6﴾ مَّآ أَفَآءَ اَ۬للَّهُ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ مِنْ أَهْلِ اِ۬لْقُرَىٰ فَلِلَّهِ
وَلِلرَّسُولِ وَلِذِي اِ۬لْقُرْبَىٰ وَالْيَتَٰمَىٰ وَالْمَسَٰكِينِ وَابْنِ اِ۬لسَّبِيلِ
كَيْ لَا يَكُونَ دُولَةَۢ بَيْنَ اَ۬لْأَغْنِيَآءِ مِنكُمْۖ وَمَآ ءَاتَىٰكُمُ اُ۬لرَّسُولُ
فَخُذُوهُۖ وَمَا نَهَىٰكُمْ عَنْهُ فَانتَهُواْۖ وَاتَّقُواْ اُ۬للَّهَۖ إِنَّ اَ۬للَّهَ
شَدِيدُ اُ۬لْعِقَابِۖ ﴿7﴾ لِلْفُقَرَآءِ اِ۬لْمُهَٰجِرِينَ اَ۬لَّذِينَ أُخْرِجُواْ
مِن دِيَٰرِهِمْ وَأَمْوَٰلِهِمْ يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِّنَ اَ۬للَّهِ وَرِضْوَٰنًا
وَيَنصُرُونَ اَ۬للَّهَ وَرَسُولَهُۥٓۖ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ اُ۬لصَّٰدِقُونَۖ ﴿8﴾ وَالَّذِينَ تَبَوَّءُو
اُ۬لدَّارَ وَالْإِيمَٰنَ مِن قَبْلِهِمْ يُحِبُّونَ مَنْ هَاجَرَ إِلَيْهِمْ وَلَا يَجِدُونَ
فِي صُدُورِهِمْ حَاجَةً مِّمَّآ أُوتُواْ وَيُوثِرُونَ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ وَلَوْ كَانَ
بِهِمْ خَصَاصَةٌۖ وَمَنْ يُّوقَ شُحَّ نَفْسِهِۦ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ اُ۬لْمُفْلِحُونَۖ ﴿9﴾

4. Wancanenku saboda haƙiƙa sun saɓawa Allah da ma'aikinsa, duk wanda ya saɓawa Allah to haƙiƙa Ubangiji mai tsananin uƙubane (gareshi).

5. Duk abinda kuka yanke (Yaku Musulmi) na dabinuwa ko kuka barta a tsaye a kan asalanta to da izinin Allah ne (ya baku zaɓi a cikin wannan,) kuma don Yakunyatar dayahudawa (da izini a cikin yankewa, a cikin tarar nunfashinsu, da cewa yankan itaciya barna ne.)

MENENE FAI'U - WATO GANIMAR YAKI DATA SAMU BADA VAHALAR MAYAkA BA MENENE HUKUNCINSA?)

6.Abinda Allah yakomo dashi bisa ma'aikinsa daga garesu, (wato Fai'u ganimar yaƙi, ganimar data samu bada wahalar yaƙi ba,) bakuyi gaggawa a kansa na wajen dawakai ko raƙuma ba, (ai baku gamu da wahala a cikinsa ba,) sai Allah dai ya sallaɗa manzanninsa a bisa wanda yaga dama, Ubangiji mai ikone bisa komai (to bakuda haƙƙi a cikinsa. Annabi Sallallahu alaihi wasallama zai keɓanta dashi, da waɗanda aka anbata a cikin aya ta biyu na daga dangogi guda huɗu, a bisa abinda ya kasance yana rabashi na daga cewa kowane ɗaya daga garesu yana da humisin humusi wato biyamin biyami (Wato ɗaya bisa biyar ɗin humusi ko ɗaya bisa ashirin da biyar). Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama yana da ragowar, yana aikata abinda yaga dama a cikinsa, zai bawa Muhajirat daga gareshi, da mutane uku daga cikin Ansaru, saboda talaucinsu.)


(UMARNIN ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA UMARNIN ALLAH NE, HANIN SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAMA HANIN ALLAH NE)

7. Abinda Allah yakoma dashi ga Manzonsa na daga mazowa alƙaryu, (kamar Safara'u da Wadil ƙura da yan-bu-A) to na Allah ne, (yana umarni cikinsa da abinda yaga dama) kuma na ma'aikin Allah ne, (Sallallahu alaihi wasallama, wato ma'abota zumuncin Annabi Sallallahu alaihi wasallama na Bani Hashim da Bani Muɗɗalib a gurin Imamuna Shafi'i Allah ya ƙara masa yarda, a wajen Maliki na Bani Hashim ne kawai) da marayu (waɗanda iyayensu suka mutu alhali su suna matalauta) da miskinai mazowa buƙatada ɗan tafarki (wanda ya yanke a cikin tafiyarsa, wato Annabi Sallallahu alaihi wasallama ya cancanceshi da waɗannan bisa abinda ya kasance yana rabashi shine cewa kowane ɗaya daga huɗun nan suna da biyamin biyamin, ragowa yana ga ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wasallama,) ana yin hakane don kada Fai'u ya zama gare tsakanin mawadata, abinda Manzon Allah ya baku (Sallallahu alaihi wasallama) na daga Fai'u to ku riƙeshi, abinda ya haneku ga buransa to ku hanu (wannan aya ta tara dukkan lamura na addini. Sawi yace "duk abinda Annabi yayi umarni dashi umarnine na Allah kuma dukkan abinda ya hana hanine na Allah).

(FALALAR MUHAJIRAI DA SAHABBAI DUKKANSU DA WASUN DA SUKABI SU DA KYAUTATAWA IZUWA RANAR ALƘIYAMA)

8. Yi mamaki ga Fukara'u masuyin Hijira, waɗanda aka fishshesu daga gidajensu da dukiyoyinsu suna neman falala daga Ubangijinsu da yardarsa suna taimakon Allah suna taimakon manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama,) waɗancanenka sune magasgata cikin imaninsu.

9. Waɗanda suke zaune a Madina suka ƙudure imani (sune Muhajirai) tun gabansu, suna son wanda yayi Hijira garesu, yayi ƙaura, basa hassada da abinda ya basu, (wato =



وَالَّذِينَ جَآءُو مِنۢ بَعْدِهِمْ يَقُولُونَ رَبَّنَا اغْفِرْ لَنَا وَلِإِخْوَانِنَا
الَّذِينَ سَبَقُونَا بِالْإِيمَانِ وَلَا تَجْعَلْ فِي قُلُوبِنَا غِلًّا لِّلَّذِينَ ءَامَنُوا۟
رَبَّنَا إِنَّكَ رَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿10﴾ * أَلَمْ تَرَ إِلَى الَّذِينَ نَافَقُوا۟
يَقُولُونَ لِإِخْوَانِهِمُ الَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِنْ أَهْلِ الْكِتَٰبِ
لَئِنْ أُخْرِجْتُمْ لَنَخْرُجَنَّ مَعَكُمْ وَلَا نُطِيعُ فِيكُمْ أَحَدًا أَبَدًا
وَإِن قُوتِلْتُمْ لَنَنصُرَنَّكُمْ وَاللَّهُ يَشْهَدُ إِنَّهُمْ لَكَٰذِبُونَ ﴿11﴾
لَئِنْ أُخْرِجُوا۟ لَا يَخْرُجُونَ مَعَهُمْ وَلَئِن قُوتِلُوا۟ لَا يَنصُرُونَهُمْ
وَلَئِن نَّصَرُوهُمْ لَيُوَلُّنَّ الْأَدْبَٰرَ ثُمَّ لَا يُنصَرُونَ ﴿12﴾ لَأَنتُمْ
أَشَدُّ رَهْبَةً فِي صُدُورِهِم مِّنَ اللَّهِ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ قَوْمٌ
لَّا يَفْقَهُونَ ﴿13﴾ لَا يُقَٰتِلُونَكُمْ جَمِيعًا إِلَّا فِي قُرًى مُّحَصَّنَةٍ
أَوْ مِن وَرَآءِ جُدُرٍۭ بَأْسُهُم بَيْنَهُمْ شَدِيدٌ تَحْسَبُهُمْ جَمِيعًا
وَقُلُوبُهُمْ شَتَّىٰ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ قَوْمٌ لَّا يَعْقِلُونَ ﴿14﴾ كَمَثَلِ
الَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ قَرِيبًا ذَاقُوا۟ وَبَالَ أَمْرِهِمْ وَلَهُمْ عَذَابٌ
أَلِيمٌ ﴿15﴾ كَمَثَلِ الشَّيْطَٰنِ إِذْ قَالَ لِلْإِنسَٰنِ اكْفُرْ فَلَمَّا كَفَرَ
قَالَ إِنِّي بَرِيٓءٌ مِّنكَ إِنِّيٓ أَخَافُ اللَّهَ رَبَّ الْعَٰلَمِينَ ﴿16﴾

= abinda Annabi ya barwa Muhajirai) suna fifitawa 'yan uwansu a kan kansu, (wađanda sukazo daga bayansu,) koda akwai buƙata a garesu izuwa abinda suka fifita wanin dashi wanda aka kiyasheshi kwađayin kansa (wato kwađayin kansa a kan dukiya wađancanenka sune haƙiƙanin marabauta.

10. Wađanda sukazo bayan Muhajirai da Ansaru suna cewa Ya Ubangijinmu! kayi gafara garemu da 'yan uwanmu wađanda suka rigayemu da imani, kadaka sanya gilli wato riƙo a zuciya ga wađanda suka bada gaskiya ya Ubangijinmu! haƙiƙa kai mai jinƙaine mai rahama ne.

(HAKANA MUNAFUƘAI DA YAHUDAWA SUKE DA SAKAMAKONSU)

11. Shin baka duba ba izuwa wađannan da sukayi munafunci, suna fada ga 'yan uwansu wađanda suka kafirta daga mazowa littafi (sune Baninnaliri da 'yan uwansu a kafirci,) Wallahi in an fiddaku ,daga Madina, lallai zamu fita taredaku ,bazamu bi wani mutum a cikinta ba daku ,ba har abada. Wallahi in an yaƙeku lallai zamu taimake ku, Allah kuwa ya tabbata lallai su maƙaryata ne.

12. Wallahi in an fitar dasu bazasu fita taredasu ba, Wallahi in an yaƙesu bazasu taimakesu ba, Wallahi in sunzo don taimakonsu, lallai zasu girka da baya aguje. Sannan baza a taimakisu Yahudawan ba (wato Allah bazai taimakesu ya hana musu azabar Ubangiji ba).

13. Haƙiƙa ku kunfi tsananin bada tsoro a cikin zukatan munafikai daga Allah (saboda jinkirin azabarsa,) wancanenka saboda su munafikai mutane ne da basa fahintar (girman Allah).

14. Bazasu yaƙeku suna tattare ba, sai dai cikin alƙaryu ababan katangancewa, ko daga bayan katangu, yaƙinsu tsakaninsu mai tsanani ne, kana zatonsu a dunƙule amma zukatansu daban daban ne, (sabanin zatonka,) wancanenka saboda haƙiƙa su mutane ne da basa hankaltar (girman Ubangiji.)

15.(Misalinsu a cikin barin imani) kamar misalin wađanda suke gabansune nan kusa (sune mushirkai ahlil Badrin), sun đanđani kuđar al'amarinsu (a duniya na kisa da waninsa), azaba mai rađađi ta tabbata garesu (a lahira).

(MALAMI WANDA ALLAH BAI ANFANESHI DA ILIMINSA BA) ULAMA' USSU'I (WATO MALAMAN DUNIYA)

16.(Misalinsu haryau a cikin sauraronsu daga munafikai da kuma jinkirinsu ga burinsu) kamar misalin Shaiđan ne lokacin dayace da mutum (Birsisa al abidi) "Zamo kafiri" a yayin daya kafirta sai yace "Ni ba ruwana dakai haƙiƙa ni ina jin tsoron Allah Ubangijin talikai" (don ƙarya da riya).

فَكَانَ عَاقِبَتَهُمَا أَنَّهُمَا فِي النَّارِ خَالِدَيْنِ فِيهَا
وَذَٰلِكَ جَزَآؤُا الظَّالِمِينَ (17) يَا أَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُوا اتَّقُوا اللَّهَ
وَلْتَنظُرْ نَفْسٌ مَّا قَدَّمَتْ لِغَدٍ وَاتَّقُوا اللَّهَ إِنَّ اللَّهَ
خَبِيرٌ بِمَا تَعْمَلُونَ (18) وَلَا تَكُونُوا كَالَّذِينَ
نَسُوا اللَّهَ فَأَنسَاهُمْ أَنفُسَهُمْ أُولَٰئِكَ هُمُ الْفَاسِقُونَ (19)
لَا يَسْتَوِي أَصْحَابُ النَّارِ وَأَصْحَابُ الْجَنَّةِ أَصْحَابُ الْجَنَّةِ
هُمُ الْفَائِزُونَ (20) لَوْ أَنزَلْنَا هَٰذَا الْقُرْءَانَ عَلَىٰ جَبَلٍ
لَّرَأَيْتَهُ خَاشِعًا مُّتَصَدِّعًا مِّنْ خَشْيَةِ اللَّهِ وَتِلْكَ
الْأَمْثَالُ نَضْرِبُهَا لِلنَّاسِ لَعَلَّهُمْ يَتَفَكَّرُونَ (21) هُوَ اللَّهُ
الَّذِي لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ عَالِمُ الْغَيْبِ وَالشَّهَادَةِ هُوَ
الرَّحْمَٰنُ الرَّحِيمُ (22) هُوَ اللَّهُ الَّذِي لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ الْمَلِكُ
الْقُدُّوسُ السَّلَامُ الْمُؤْمِنُ الْمُهَيْمِنُ الْعَزِيزُ الْجَبَّارُ الْمُتَكَبِّرُ
سُبْحَانَ اللَّهِ عَمَّا يُشْرِكُونَ (23) هُوَ اللَّهُ الْخَالِقُ
الْبَارِئُ الْمُصَوِّرُ لَهُ الْأَسْمَاءُ الْحُسْنَىٰ يُسَبِّحُ لَهُ
مَا فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ وَهُوَ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ (24)

17. To sai ƙarshensu su biyu (abin halakarwa da wanda ya halakar dashi sai ƙarshensu) ya kasance cewa suna wuta madawwama. Wancanenka shine sakamakon kafirai (wato azzalumai).

(MASU WAJABTA TSORON ALLAH DA WANI ABU DAGA ASMA'ULLAHIL HUSNA) (MALAMAN LAHIKA DA MALAMAN ALLAH)

18. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! Kuji tsoron Allah (a muƙamin ku malmoni) kowace rai ta duba abindata gabatar saboda ranar lahira kuji tsoron Allah a (Muƙaminku na Ihsani) haƙiƙa Ubangiji masanine da abinda kuke aikatawa.

19. Kadaku ,zamo kamar waɗannan da suka manta Allah (Subhanay hu wa ta'ala, suka bar anbatonsa da biyayya tasa) ya mantar dasu kawukansu. wadancanenka sune haƙiƙanin fasiƙai.

20. 'Yan wuta da 'yan Aljanna baza suyi daidai ba, 'yan Aljanna sune haƙiƙanin masu rabauta.

21. Da zamu saukar da wannan Alƙur'ani a kan dutse da ka ganshi yana mai tawali'u yana mai kyakykecewa don tsoron Allah. Wadancanenka misalce misalce muna sabata ga mutane (masu hankali) donsuyi tunani (su bada gaskiya). (Wani Abu Daga Asma'-Ullahil Husna)

22. Shine Allah wanda babu abin bautawa da gaskiya saishi, masanin asirin fake dana sarari shine mai ni'imtawa da manya manyan ni'imomi da siraran ni'imomi.

23. Shine Allahu wanda babu abin bautawa da gaskiya saishi, mai cikakken tasrifi a cikin halitta na samarwa da rasarwa, mai tsarkaka ga buran abinda bai kamace shi ba mai zama sumul ga buran abinda yake na tawaya, mai gasgata manzanninsa da halittar mu'ujuza a garesu, kuma mai gasgata muminal da imaninsu da ikhlasinsu, (saboda ba mai tsinkaye a kan ikhlasi sai Allah,) mai la'akari da aikin bayinsa,.mai ganinsu basa ganinsa, mabuwayi, mai dole, (wato ya tilashi bayinsa bisa abinda yake nufi), mai girmama ga buran abinda bai kamace shi ba. Tsarki ya tabbatarwa Ubangiji ga buran abinda suke shirkantawa dashi.

24. Shine Allah mahalicci mai samar da talikai daga rashi, mai bayyana zatoti daga rashi izuwa samuwa, (wato mai ƙago surori a bisa gwargwadon abinda ya nufa yaba kowane ɗaya daga halitta sura keɓantacciya da yanayi madaidaici wanda zai banbanta dashi), abinda yake sammai da ƙassai yana gaisheshi shine mabuwayi, shine mai hikima.

60 سُورَةُ المُمتَحنَة مَدنِيّة
وَهِيَ ثَلاثَ عَشرَةَ ءَايَة 13

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

ثمن

* يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّخِذُواْ عَدُوِّي وَعَدُوَّكُمْ أَوْلِيَآءَ تُلْقُونَ إِلَيْهِم بِٱلْمَوَدَّةِ
وَقَدْ كَفَرُواْ بِمَا جَآءَكُم مِّنَ ٱلْحَقِّ يُخْرِجُونَ ٱلرَّسُولَ وَإِيَّاكُمْ
أَن تُؤْمِنُواْ بِٱللَّهِ رَبِّكُمْ إِن كُنتُمْ خَرَجْتُمْ جِهَٰدًا فِي سَبِيلِي وَٱبْتِغَآءَ
مَرْضَاتِي تُسِرُّونَ إِلَيْهِم بِٱلْمَوَدَّةِ وَأَنَا أَعْلَمُ بِمَا أَخْفَيْتُمْ وَمَا أَعْلَنتُمْ وَمَن يَفْعَلْهُ
مِنكُمْ فَقَدْ ضَلَّ سَوَآءَ ٱلسَّبِيلِ ﴿1﴾ إِن يَثْقَفُوكُمْ يَكُونُواْ لَكُمْ أَعْدَآءً وَيَبْسُطُوٓاْ
إِلَيْكُمْ أَيْدِيَهُمْ وَأَلْسِنَتَهُم بِٱلسُّوٓءِ وَوَدُّواْ لَوْ تَكْفُرُونَ ﴿2﴾ لَن تَنفَعَكُمْ
أَرْحَامُكُمْ وَلَآ أَوْلَٰدُكُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ يَفْصِلُ بَيْنَكُمْ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ
بَصِيرٌ ﴿3﴾ قَدْ كَانَتْ لَكُمْ إِسْوَةٌ حَسَنَةٌ فِي إِبْرَٰهِيمَ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ إِذْ قَالُواْ
لِقَوْمِهِمْ إِنَّا بُرَءَٰٓؤُاْ مِنكُمْ وَمِمَّا تَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ كَفَرْنَا بِكُمْ وَبَدَا بَيْنَنَا وَبَيْنَكُمُ
ٱلْعَدَٰوَةُ وَٱلْبَغْضَآءُ أَبَدًا حَتَّىٰ تُؤْمِنُواْ بِٱللَّهِ وَحْدَهُۥٓ إِلَّا قَوْلَ إِبْرَٰهِيمَ لِأَبِيهِ
لَأَسْتَغْفِرَنَّ لَكَ وَمَآ أَمْلِكُ لَكَ مِنَ ٱللَّهِ مِن شَيْءٍ رَّبَّنَا عَلَيْكَ تَوَكَّلْنَا وَإِلَيْكَ أَنَبْنَا وَإِلَيْكَ
ٱلْمَصِيرُ ﴿4﴾ رَبَّنَا لَا تَجْعَلْنَا فِتْنَةً لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ وَٱغْفِرْ لَنَا رَبَّنَآ إِنَّكَ أَنتَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿5﴾

Wannan Sura Itace Suratul Mumtihanati

A Madina aka saukar da ita aya goma sha uku ce (13)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan sura ta iyakance matsayin musulmi daga mushurkai, da iyakancewa cikakke wajen soyayya da saduwa da nahiyarsu da ƙanƙan dakai da nahiyar alaƙa ta aurantakaiya, wacce take tsaye tsakanin Musulmi da waninsa da yadda manzon Allah yayi mubaya'a da mata, an rufe tada buran dasheseniya da kafirai kamar yadda surar ta fara da haka.

(DASHESHENIYA DA KAFIRAI DA ALAƘARMU DASU)

1. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! kada ku ,riƙi magaucina magaucinku (kafiran Makka) masoya, kuna saduwa izuwa garesu da soyayya tsaninku dasu (wato Annabi Sallallahu alaihi wasallama yayi nufin yaƙinsu wanda ya ɓoyeshi izuwa gareku ya bada Dungu da yaƙin Hunainu, Khaɗibu ɗan Abu Baltata, ya rubuta takarda garesu da waɗancanenka saboda abinda yake garesu nasa na'ya'yaye da iyali mushurkai, sai manzon Allah ya nemi komo da takarda daga wanda ya aikeshi tareda ita, ta wajen sanarwar da wannan ya Karɓi hanzarin Khaɗibu da wannan ɗin) haƙiƙa sun kafirce da abinda yazo muku na gaskiya (addinin Musulunci da Alƙur'ani) suna fitar da manzo daku ,(daga Makka saboda ƙuntatawarsu a gareku), don kun bada gaskiya da Allah Ubangijinku, in kun zamo ku kun fita ga yaƙi saboda Allah da neman yarda tasa (to kadaku ,riƙesu waliyyai ko majiɓinta,) kuna asirtawa garesu da soyayya, ni masanine da abinda kuka ɓoye da abinda kuka bayyana, wanda ya aikatashi daga cikinku, (wato asirta labarin Annabi Sallallahu alaihi wasallama) haƙiƙa ya ɓacewa hanya madaidaiciya.
2. In suka dace daku ,sa zama magauta gareku, sa shimfiɗe hannayensu gareku (da kisa da duka, sa shimfiɗe) harasansu da miyagun sunaye, burinsu ku zama kafirai.
3. Zumunce-zumuncenku basu anfaneku ba, wato 'ya'yayenku (mushurkai, waɗanda saboda sune kuka asirta labarin, to basu anfaneku daga azabar lahira ba) ranar Lahira ake rarrabe hukunci tsakaninku, da tsakaninsu, (ku zamo a cikin aljanna su kuma su zamo cikin wuta) Allah masanine da abinda kuke aikatawa.

(ADDININ WAƊANDA SUKE GABANMU ADDININMUNE MUDDAR HANI BAI AFKU BA)

4. Haƙiƙa kwaikwayo kyakkyawa ya tabbata gareku cikin Ibrahim (kwaikwayonsa cikin magana da aiki) da waɗanda suke taredashi (na daga muminai, tarayya ta ban gaskiya da gasgatawa), lokacin da suka faɗa ga mutanensu haƙiƙa mu makuɓuta ne daga gareku da abinda kuke bautawa ba Allah ba, mun kafirce daku, ƙiyayya ta bayyana tsakaninmu daku ,har abada, sai kun bada gaskiya da Allah shi kaɗai. Sai faɗin Ibrahimu (Alaihissalamu) ga babansa (ko baffansa,) lallai zan nema maka gafarar Ubangijina, ni bazan mallaki komai na sakamako ko na azaba daga Ubangiji ba a gareka Ya Ubangiji gareka muke dogara izuwa gareka muka koma, makoma tana gareka kai kaɗai.
5. Sukace: "Ubangiji! Kadaka sanyamu fitina ga waɗanda suka kafirta, (wato kadaka rinjayar dasu a kanmu su zaci cewasu a kan gaskiya suke, don kadasu fitintu, hankulansu su tafi tareda mu) kayi gafara garemu Ya Ubangijinmu! haƙiƙa kaine mabuwayi gwani (a cikin aikinka.")

لَقَدْ كَانَ لَكُمْ فِيهِمْ أُسْوَةٌ حَسَنَةٌ لِّمَن كَانَ يَرْجُوا۟ ٱللَّهَ وَٱلْيَوْمَ ٱلْءَاخِرَ
وَمَن يَتَوَلَّ فَإِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْغَنِىُّ ٱلْحَمِيدُ ۝٦ ۞ عَسَى ٱللَّهُ أَن يَجْعَلَ بَيْنَكُمْ
وَبَيْنَ ٱلَّذِينَ عَادَيْتُم مِّنْهُم مَّوَدَّةً وَٱللَّهُ قَدِيرٌ وَٱللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ۝٧
لَّا يَنْهَىٰكُمُ ٱللَّهُ عَنِ ٱلَّذِينَ لَمْ يُقَٰتِلُوكُمْ فِى ٱلدِّينِ وَلَمْ يُخْرِجُوكُم
مِّن دِيَٰرِكُمْ أَن تَبَرُّوهُمْ وَتُقْسِطُوٓا۟ إِلَيْهِمْ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلْمُقْسِطِينَ ۝٨
إِنَّمَا يَنْهَىٰكُمُ ٱللَّهُ عَنِ ٱلَّذِينَ قَٰتَلُوكُمْ فِى ٱلدِّينِ وَأَخْرَجُوكُم مِّن
دِيَٰرِكُمْ وَظَٰهَرُوا۟ عَلَىٰٓ إِخْرَاجِكُمْ أَن تَوَلَّوْهُمْ وَمَن يَتَوَلَّهُمْ فَأُو۟لَٰٓئِكَ
هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ۝٩ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِذَا جَآءَكُمُ ٱلْمُؤْمِنَٰتُ مُهَٰجِرَٰتٍ
فَٱمْتَحِنُوهُنَّ ٱللَّهُ أَعْلَمُ بِإِيمَٰنِهِنَّ فَإِنْ عَلِمْتُمُوهُنَّ مُؤْمِنَٰتٍ
فَلَا تَرْجِعُوهُنَّ إِلَى ٱلْكُفَّارِ لَا هُنَّ حِلٌّ لَّهُمْ وَلَا هُمْ يَحِلُّونَ لَهُنَّ
وَءَاتُوهُم مَّآ أَنفَقُوا۟ وَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ أَن تَنكِحُوهُنَّ إِذَآ ءَاتَيْتُمُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ
وَلَا تُمْسِكُوا۟ بِعِصَمِ ٱلْكَوَافِرِ وَسْـَٔلُوا۟ مَآ أَنفَقْتُمْ وَلْيَسْـَٔلُوا۟ مَآ أَنفَقُوا۟
ذَٰلِكُمْ حُكْمُ ٱللَّهِ يَحْكُمُ بَيْنَكُمْ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ۝١٠
وَإِن فَاتَكُمْ شَىْءٌ مِّنْ أَزْوَٰجِكُمْ إِلَى ٱلْكُفَّارِ فَعَاقَبْتُمْ فَـَٔاتُوا۟ ٱلَّذِينَ ذَهَبَتْ
أَزْوَٰجُهُم مِّثْلَ مَآ أَنفَقُوا۟ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ ٱلَّذِىٓ أَنتُم بِهِۦ مُؤْمِنُونَ ۝١١

ربع

6. Haƙiƙa kwaikwayo kyakkyawa ya tabbata gareku (ya al'ummata Muhammadin Sallallahu alaihi wasallama) ga wanda ya kasance yana ƙaunar Allah da ranar lahira. Wanda yajiɓinci kafirai, haƙiƙa Ubangiji mawadaci ne abin godewa da ɗa'a tasa.
7. Ana ƙaunar Ubangiji ya sanya soyayya tsakaninku da waɗanda kuke gabadasu (na daga kafiran Makka don ɗa'a ga Allah, shine ya shiryesu da imani, su zama masoya a gareku majiɓinta,) Ubangiji mai ikone (bisa haka, an aikata wannan bayan buɗe Makka,) Ubangiji mai gafara ne (garesu bisa abinda ya wuce,) mai jinƙaine (gareku.)
8. Allah baya hana ku ga buran waɗannan da basu yaƙeku ba(na daga kafirai) a cikin addini, basu fitar daku ,daga gidaddajinku, baya hanaku kuyi biyayya garesu kusadu izuwa garesu da adalci, (to wannan gabannin umarni da yaƙinsu ne) haƙiƙa Ubangiji yana son masuyin adalci.
9. Kaɗai dai Ubangiji yana hanaku ga buran waɗannan da suka yaƙeku a cikin addini suka fitar daku ,daga gidaddajinku, sukayi taimako kan fitar daku, yana hanaku ɗasawa dasu, duk wanda yaɗasa dasu haƙiƙa sune azzalumai.

(MATAYE MASU HIJIRA DA CAFFA DASU)

10.Yaku waɗanda suka bada gaskiya! idan muminai mata waɗanda suka bada gaskiya da harshensu sukazo muku suna masu Hijira daga kafirai (bayan sulhu da akayi dasu a Hudebiyya, a kan cewa wanda yazo musu daga cikinsu izuwa muminai za a mai dashi,) ku jarrabesu (da rantsuwa cewasu basu fita ba sai don kwaɗayi cikin Musulunci, ba don ƙin mazajensu kafirai ba, ba don bege ga mazaje na Musulmi ba, hakanan Annabi Sallallahu alaihi wasallama ya kasance yana rantsar dasu,) Allah ne masani da imaninsu, to in kuka zacesu muminai (saboda rantsuwar nan,) to kadaku ,maishesu izuwa kafirai, su matan nan ba halal ne gasu waɗannan mazaje ba, su kuma mazajen bazasu halatta ga matayen ba, kuma kuba mazajensu kafirai daga abinda suka ciyar a bisa matayen na sadaki, babu laifi a garesu ku auresu (da sharaɗinsa shine ƙarewar iddarsa a cikin Musulunci da waliyyi da shaidu da sauransu) in kun basu sadakansu na matayen, kada kuyi riƙo da igiyar auren mataye kafirai (saboda Musuluncinku ya yanketa ita igiyar wala waɗanda suka riskuda mushirkan alhali sunyi ridda, saboda yankewar igiyar auren naku saboda riddatasu,) ku nemi abinda kuka ciyar (a kansu na daga sadakai a cikin surorin riddar) ku nema daga waɗanda suka auresu na daga kafirai,) su kuma mazajen su nemi abinda suka ciyar (bisa matayen da sukayi Hijira, wato muhajirai mataye, tamfar daya gabatacewa su za a basu shi) wancanenku hukuncin Allah ne dayayi hukunci tsakaninku, Ubangiji masani ne, gwani.
11. Idan wani abu daga matayenku ya tsere muku izuwa kafirai (suna masu ridda) ku kayi yaƙi, kukayi riba, to kuba waɗanda matayensu suka tafi na daga ganima misalin abinda suka ciyar, (don saboda tserewarsa garesu daga jihar kafirai) kuji tsoron Allah wandaku ,kuka bada gaskiya dashi, (haƙiƙa muminai sun aikata abinda aka umarce su dashi, na daga miƙawa izuwa muminai da kafirai, sannan aka ɗauke wannan hukuncin)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيٓءُ إِذَا جَآءَكَ ٱلْمُؤْمِنَٰتُ يُبَايِعْنَكَ عَلَىٰٓ أَن لَّا يُشْرِكْنَ
بِٱللَّهِ شَيْـًٔا وَلَا يَسْرِقْنَ وَلَا يَزْنِينَ وَلَا يَقْتُلْنَ أَوْلَٰدَهُنَّ
وَلَا يَأْتِينَ بِبُهْتَٰنٍ يَفْتَرِينَهُۥ بَيْنَ أَيْدِيهِنَّ وَأَرْجُلِهِنَّ وَلَا يَعْصِينَكَ
فِي مَعْرُوفٍ فَبَايِعْهُنَّ وَٱسْتَغْفِرْ لَهُنَّ ٱللَّهَ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿12﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَوَلَّوْاْ قَوْمًا غَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيْهِمْ
قَدْ يَئِسُواْ مِنَ ٱلْأٓخِرَةِ كَمَا يَئِسَ ٱلْكُفَّارُ مِنْ أَصْحَٰبِ ٱلْقُبُورِ ﴿13﴾

61 سُورَةُ الصَّفِّ مَدَنِيَّة
وَهِيَ أَرْبَعَ عَشْرَةَ ءَايَة 14

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ثمن
* سَبَّحَ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلْأَرْضِ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿1﴾
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لِمَ تَقُولُونَ مَا لَا تَفْعَلُونَ ﴿2﴾ كَبُرَ مَقْتًا
عِندَ ٱللَّهِ أَن تَقُولُواْ مَا لَا تَفْعَلُونَ ﴿3﴾ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلَّذِينَ
يُقَٰتِلُونَ فِي سَبِيلِهِۦ صَفًّا كَأَنَّهُم بُنْيَٰنٌ مَّرْصُوصٌ ﴿4﴾ وَإِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِقَوْمِهِۦ
يَٰقَوْمِ لِمَ تُؤْذُونَنِي وَقَد تَّعْلَمُونَ أَنِّي رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيْكُمْ فَلَمَّا زَاغُوٓاْ
أَزَاغَ ٱللَّهُ قُلُوبَهُمْ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِي ٱلْقَوْمَ ٱلْفَٰسِقِينَ ﴿5﴾

12. Yakai wannan Annabi! (Sallallahu Alaika wa Sallam) Idan muminai mata sukazo maka suna cafta dakai a kan bazasu ƙara shirka da Allah ba, baza suyi sata ba, baza suyi zina ba, bazasu kashe 'ya'yansu ba (tamfar da akeyi a Jahiliyya, shine binne 'ya'ya mata da ransu, don tsoron talauci da la'ari) bazasu zoda ƙuce ba dasuke ƙagensa nan ga hannuwansu da ƙafafunsu, (wato ɗan tsuntuwa, an sifanta shi da dana hakika, don saboda ita uwar in ta ajiye shi sai ya faɗa tsakanin hannayenta da ƙafafuwanta) bazasu saɓeka a cikin aikata abin kirki ba a shari'a, (wato abinda yake da ɗa'ar Allah kamar barin kukan kera da kerketa tufa, da cisge gasu da keta aljihu da yakushe fuska,) to kayi mubaya'a dasu, (manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama ya aikata wannan da magana ba musafaha da ɗaya daga cikinsu ba,) nemi gafarar Allah garesu, haƙiƙa Allah mai gafara ne mai rahama.

13. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya! kadaku ,kusanci mutane da Allah yayi fushi a garesu (sune Yahudu) haƙiƙa sun ɗebe haso daga sakamakon Lahira (tareda sakan kancewarsu da ita, saboda takadarancin da sukayiwa ma'aikin Allah (Sallallahu alaihi wasallama tareda saninsu da gaskiya tasa,) tamfar da kafiran suka ɗebe haso daga ma'abota Raburbura (daga alherin lahira zamanin da ake bijirar musu da kujerunsu na gidan Aljanna, dasun bada gaskiya, ko abinda suke komowa a gareshi na wuta.)

Wannan Sura Itace Suratul Saffi

A Madina aka saukar da ita aya goma sha hudùce (14).

Ina farawa dasunan Ubangiji mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(wannan sura ta ƙunshi faɗakar da ba'alin abinda ya wajaba a kansu da basu tsoro da kadasu zama kamar mutanen Annabi Musa tareda bayanin cewa Musulunci shine addinin Allah, cewa kuma shine mai rinjaye kan addinai, sannan kuma sanya hanya mai'aikewa izuwa shiriya.)

1. Abinda yake cikin sammai da abinda yake cikin ƙassai sun tsarkake Ubangiji, shine mabuwayi (cikin mulkinsa) gwani cikin (aikinsa).

2.Yaku waɗanda suka bada gaskiya! donme kuke faɗin abinda bazaku aikata (shi) ba (yayin da kuka risba a Uhudu bayan kun nemi yin jihadi?).

(WAJABCIN HAƊINKAN MUSULMI) WAHDATUL ISLAMI

3. Ya girma zargi a gurin Allah ku faɗi abinda bazaku aikata ba.

(CUTAR ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAM KAFIRCI NE)

4. Haƙiƙa Ubangiji yana son waɗanda suke yaƙi a cikin inganta addininsa suna masu yin sahu-sahu, kai kace ginine abin danfarawa.

5. Ka ambata zamanin da Annabi Musa yake faɗawa mutanensa"Yaku mutanena! donme kuke cutata? (Sunce wai shi yana da kayan maza, bako haka ba ne, kuma sun ƙaryata shi,) lallai kun san haƙiƙa ni manzon Allah ne izuwa gareku, (jakada ko girmama shi ake.)" Zamanin da suka karkace (ga buran gaskiya da cutarsa,) sai Allah ya karkatar da zukatansu (ga buran shiriya, bisa daidai da abinda Allah ya ƙaddara tun azal,) Allah baya shiriyar mutane fasiƙai, (wato kafirai cikin saninsa.)

وَإِذْ قَالَ عِيسَى ابْنُ مَرْيَمَ يَٰبَنِي إِسْرَآءِيلَ إِنِّي رَسُولُ اللَّهِ إِلَيْكُم مُّصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ
يَدَيَّ مِنَ التَّوْرَىٰةِ وَمُبَشِّرًا بِرَسُولٍ يَأْتِي مِنْ بَعْدِي اسْمُهُ أَحْمَدُ فَلَمَّا جَآءَهُم
بِالْبَيِّنَٰتِ قَالُوا هَٰذَا سِحْرٌ مُّبِينٌ ﴿6﴾ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ افْتَرَىٰ عَلَى اللَّهِ الْكَذِبَ وَهُوَ
يُدْعَىٰ إِلَى الْإِسْلَٰمِ وَاللَّهُ لَا يَهْدِي الْقَوْمَ الظَّٰلِمِينَ ﴿7﴾ يُرِيدُونَ لِيُطْفِئُوا نُورَ اللَّهِ
بِأَفْوَٰهِهِمْ وَاللَّهُ مُتِمٌّ نُّورَهُ وَلَوْ كَرِهَ الْكَٰفِرُونَ ﴿8﴾ هُوَ الَّذِي أَرْسَلَ
رَسُولَهُ بِالْهُدَىٰ وَدِينِ الْحَقِّ لِيُظْهِرَهُ عَلَى الدِّينِ كُلِّهِ وَلَوْ كَرِهَ الْمُشْرِكُونَ ﴿9﴾
يَٰأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُوا هَلْ أَدُلُّكُمْ عَلَىٰ تِجَٰرَةٍ تُنجِيكُم مِّنْ عَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿10﴾
تُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ وَرَسُولِهِ وَتُجَٰهِدُونَ فِي سَبِيلِ اللَّهِ بِأَمْوَٰلِكُمْ وَأَنفُسِكُمْ
ذَٰلِكُمْ خَيْرٌ لَّكُمْ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿11﴾ يَغْفِرْ لَكُمْ ذُنُوبَكُمْ
وَيُدْخِلْكُمْ جَنَّٰتٍ تَجْرِي مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَٰرُ وَمَسَٰكِنَ طَيِّبَةً فِي جَنَّٰتِ
عَدْنٍ ذَٰلِكَ الْفَوْزُ الْعَظِيمُ ﴿12﴾ وَأُخْرَىٰ تُحِبُّونَهَا نَصْرٌ مِّنَ اللَّهِ
وَفَتْحٌ قَرِيبٌ وَبَشِّرِ الْمُؤْمِنِينَ ﴿13﴾ يَٰأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُوا كُونُوا أَنصَارًا لِّلَّهِ
كَمَا قَالَ عِيسَى ابْنُ مَرْيَمَ لِلْحَوَارِيِّينَ مَنْ أَنصَارِي إِلَى اللَّهِ قَالَ الْحَوَارِيُّونَ
نَحْنُ أَنصَارُ اللَّهِ فَـَٔامَنَت طَّآئِفَةٌ مِّنۢ بَنِي إِسْرَآءِيلَ وَكَفَرَت طَّآئِفَةٌ
فَأَيَّدْنَا الَّذِينَ ءَامَنُوا عَلَىٰ عَدُوِّهِمْ فَأَصْبَحُوا ظَٰهِرِينَ ﴿14﴾

(ALBISHIR DA MANZON ALLAH ALLALLAHU ALAIHI WA SALLAM DAGA ANNABI ISA ALAIHI SSALAM)

6. Ka ambata zamanin da Annabi Isa Ibini Maryama (Alaihissalam) yace "Ya Bani Isra'ila (baice ya mutanena ba, don cewa shi babu zumunci tsakaninsa dasu,) ni jakadan Allah ne izuwa gareku, mai gasgatawa da.abinda yake gabana na Attaura, mai albishir da manzon dazaizo bayana sunansa Ahmad (Sallallahu alaihi wasallama") (Ubangiji yace) "zamanin da Ahmadu(Sallallahu alaihi wasallama) yazowa kafirai da alamomi sai sukace "wannan abin nan da yazo dashi tsafi ne mabayyani."
7. Babu mafi tsananin zalinci daga wanda ya ƙaga ƙarya bisa Allah(da dangana abokin tarayya da ɗa izuwa gareshi da sifanta ayoyinsa da tsafi) alhali ana kiransa izuwa Musulunci. Allah baya shiriyar mutane kafirai.

(ALBISHIRIN MU!!)

8. Suna nufin su bice hasken Ubangiji da maganganun bakunansu (cewa sihiri ne, waƙace, bokancine) Allah mai cika haskensa ne koda kafirai sunƙi (wannan).(Wannan Bishara Ce Mai Girma)
9. Shine wanda ya aiko manzonsa da shiriya da addinin gaskiya donya rinjayar dashi a kan addinai dukkansu, (waɗanda suka saɓa masa) koda mushurkai basu so ba.

(CINIKI MAI RIBA)

10. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! bana shiryar daku ,bisa ciniki da zata tserar daku ,azaba mai raɗaɗi ba? (shiryar damu).
11. (Yace) "Ku dauwama kan bada gaskiya da Allah da ma'aikinsa, kuyi yaƙi a cikin inganta addinin Allah da dukiyoyinku da kawukanku, wancanenku, shi yafi anfani a gareku in kun kasance kun san haka, (to ku aikata shi.)
12. Ya gafarta muku zunubanku, ya shigar daku ,aljannatai wacce ƙoramu suke kwarara ƙarƙashinta, da mazaunai daɗaɗa, a aljannar dauwama, wancanenka shine rabo mai girma!
13. Zai baku ni'ima da kuke sonta shine taimako daga Allah da buɗi makusanci, kaiwa muminai albishir (da nasara da buɗi.)

(SUFAYE A ZAMANIN ANNABI ISA ALAIHISSALAMU)

14. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! ku zama mataimaka ga addinin Allah, (tamfar da Hawariyawa suka kasance kamar haka,) tamfar da Isa Ibni Maryama (Alaihissalam) ya faɗa ga Hawariyawa, "su waye mataimakana izuwa addinin Allah?" Hawariya sukace "mune mataimaka Allah," (sune Sufayen Annabi Isa Alaihissalamu, sune farkon waɗanda suka bada gaskiya dashi, su goma sha biyu ne ma'abota tsananin farin tufa, Ance mawanka ne,) sai jama'a ta Bani Isra'ila ta bada gaskiya da Annabi Isa, (sukace haƙiƙa bawan Allah ne an ɗauke shi izuwa sama,) waɗansu jama'a suka kafirce (saboda faɗinsu cewa shi ɗan Allah ne ya ɗauke shi izuwa gareshi, sukayi ta husuma a junansu,) sai muka ƙarfafi waɗannan da suka bada gaskiya a kan magautansu (wato muka taimaki muminan a kan kafiran nan,) suka zamo sune masu rinjaye a kansu.

سُورَةُ الجُمُعَةِ مَدَنِيَّة 62
وَهِيَ إِحْدَىٰ عَشْرَةَ ءَايَة 11

حزب

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

* يُسَبِّحُ لِلَّهِ مَا فِي السَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي الْأَرْضِ الْمَلِكِ الْقُدُّوسِ الْعَزِيزِ
الْحَكِيمِ (1) هُوَ الَّذِي بَعَثَ فِي الْأُمِّيِّينَ رَسُولًا مِّنْهُمْ يَتْلُواْ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتِهِ
وَيُزَكِّيهِمْ وَيُعَلِّمُهُمُ الْكِتَٰبَ وَالْحِكْمَةَ وَإِن كَانُواْ مِن قَبْلُ لَفِي ضَلَٰلٍ
مُّبِينٍ (2) وَءَاخَرِينَ مِنْهُمْ لَمَّا يَلْحَقُواْ بِهِمْ وَهُوَ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ (3)
ذَٰلِكَ فَضْلُ اللَّهِ يُؤْتِيهِ مَن يَشَاءُ وَاللَّهُ ذُو الْفَضْلِ الْعَظِيمِ (4)
مَثَلُ الَّذِينَ حُمِّلُواْ التَّوْرَىٰةَ ثُمَّ لَمْ يَحْمِلُوهَا كَمَثَلِ الْحِمَارِ يَحْمِلُ أَسْفَارًا
بِئْسَ مَثَلُ الْقَوْمِ الَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِ اللَّهِ وَاللَّهُ لَا يَهْدِي الْقَوْمَ
الظَّٰلِمِينَ (5) قُلْ يَٰأَيُّهَا الَّذِينَ هَادُواْ إِن زَعَمْتُمْ أَنَّكُمْ
أَوْلِيَاءُ لِلَّهِ مِن دُونِ النَّاسِ فَتَمَنَّوُاْ الْمَوْتَ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ (6)
وَلَا يَتَمَنَّوْنَهُ أَبَدًا بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ وَاللَّهُ عَلِيمٌ بِالظَّٰلِمِينَ (7)
قُلْ إِنَّ الْمَوْتَ الَّذِي تَفِرُّونَ مِنْهُ فَإِنَّهُ مُلَٰقِيكُمْ ثُمَّ تُرَدُّونَ
إِلَىٰ عَٰلِمِ الْغَيْبِ وَالشَّهَٰدَةِ فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ (8)

Wannan Sura Itace Suratul Juma'ati
A Madina aka saukar da ita aya goma sha ɗayace (11).
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan sura ta tara falalar Allah da aiko manzon Allah Sallallahu alaihi waSallama daga Larabawa, tayi magana kan Yahudu da basu kiyaye shari'arsu ba, sannan ta zoda hikimomi a cikinta sallar, Juma'a da Zikiri Ilahi Mai yawa. Juma'a.)

1.Abinda yake sammai da ƙassai yana tsarkakewa ga Ubangiji (ma'ana yana anbatonsa,) mai cikakken tasrifi, mai tsarkaka ga abinda bai dace dashi ba mabuwayi (cikin mulkinsa,) gwani (cikin aikinsa).

(FALALAR SAHABBAI ALLAH YA ƘARA YARDA GARESU)

2. Shine wanda ya aiko manzo daga cikin Ummawa (wato larabawan Jahiliyya) (wanda akece dashi Ummiyi shine wanda baya rubutu baya karatu, shine manzon Allah (Sallallahu alaihi wa sallama) yana karantawan ayoyi a garesu, yana tsarkakesu(daga shirka,) yana sanar dasu tafsirin Alƙur'ani da abinda yake cikinsa na daga hukunce- hukunce, wanda shine hadisi. haƙiƙa sun kasance gaban zuwansa suna cikin ɓata mabayyani.

(FALALAR TABI,AI)

3. Ya aiko waɗansu a cikinsu basu risku dasu ba a cikin marigayiya na daga girma da fifika, shine mabuwayi gwani (sune tabi'ai, takaitawa a kansu yana nuna falalar Sahabbai waɗanda aka aiko Annabi cikinsu tareda bayyana fifikonsu a kan waɗanda basu ba, daga waɗanda aka aikoshi garesu suka bada gaskiya, na daga dukkan mutane da aljannu har izuwa tashin alƙiyama, domin kowane ƙarni yafi wanda yake binsa.)

4. Wancananka falalar Allah ne, yana bashe shi ga wanda yaga dama (Annabi Sallallahu alaihi wa sallama da waɗanda suke tare dashi,) Ubangiji mai falala ne mai girma.

(YAHUDAWA DA RASHIN BIYAYYARSU GA ATTAURA)

5. Misalin waɗannan da aka ɗora musu aiki da Attaura sannan basuyi aiki da ita ba (na daga siffar manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama,} kamar misalin jakine da yake dauke da kayan littattafai (a cikin rashin anfaninsa da ita,) tur da misalin mutanen da suka ƙaryata da ayoyin Allah! (wacce ta gasgata Annabi Sallallahu alaihi wasallama) Allah baya shiriyar mutane'kafirai.

(TAHADDIN BUWAYAR ALƘUR'ANI DA HANA YAHUDAWA BURIN MUTUWA HAR ZUWA YAU)

6. Cene "Yaku waɗanda kuka Yahudantu! in kun riya cewaku haƙiƙa ku masoya Allah ne ba tareda mutane ba, to ku guraci mutuwa in kun kasance magasgata."

7. Bazasu guraci mutuwa ba har abada, saboda abinda hannuwansu ta gabata (na daga kafircewa da Annabi Sallallahu alaihi wasallama wanda ya lazamunta ƙaryarsu.) Allah masanine da kafirai.

8. Cène (dasu) "haƙiƙa mutuwa wadda kuke gudu daga gareta to haƙiƙa zata haɗu dakune, sannan a maidaku ,izuwa masanin asirin fake dana sarari, sannan ya baku labari da abinda kuka kasance kuna aikatawa."

ثمن

۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا نُودِيَ لِلصَّلَوٰةِ مِن يَوْمِ ٱلْجُمُعَةِ فَٱسْعَوْاْ إِلَىٰ
ذِكْرِ ٱللَّهِ وَذَرُواْ ٱلْبَيْعَ ذَٰلِكُمْ خَيْرٌ لَّكُمْ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿9﴾ فَإِذَا قُضِيَتِ
ٱلصَّلَوٰةُ فَٱنتَشِرُواْ فِي ٱلْأَرْضِ وَٱبْتَغُواْ مِن فَضْلِ ٱللَّهِ وَٱذْكُرُواْ ٱللَّهَ
كَثِيرًا لَّعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿10﴾ وَإِذَا رَأَوْاْ تِجَٰرَةً أَوْ لَهْوًا ٱنفَضُّوٓاْ إِلَيْهَا وَتَرَكُوكَ
قَآئِمًا قُلْ مَا عِندَ ٱللَّهِ خَيْرٌ مِّنَ ٱللَّهْوِ وَمِنَ ٱلتِّجَٰرَةِ وَٱللَّهُ خَيْرُ ٱلرَّٰزِقِينَ ﴿11﴾

سُورَةُ ٱلْمُنَٰفِقُونَ مَدَنِيَّةٌ 63
وَهِيَ إِحْدَىٰ عَشْرَةَ ءَايَةً 11

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِذَا جَآءَكَ ٱلْمُنَٰفِقُونَ قَالُواْ نَشْهَدُ إِنَّكَ لَرَسُولُ ٱللَّهِ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ إِنَّكَ
لَرَسُولُهُۥ وَٱللَّهُ يَشْهَدُ إِنَّ ٱلْمُنَٰفِقِينَ لَكَٰذِبُونَ ﴿1﴾ ٱتَّخَذُوٓاْ
أَيْمَٰنَهُمْ جُنَّةً فَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ إِنَّهُمْ سَآءَ مَا كَانُواْ
يَعْمَلُونَ ﴿2﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ ءَامَنُواْ ثُمَّ كَفَرُواْ فَطُبِعَ عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ
فَهُمْ لَا يَفْقَهُونَ ﴿3﴾ وَإِذَا رَأَيْتَهُمْ تُعْجِبُكَ أَجْسَامُهُمْ وَإِن يَقُولُواْ
تَسْمَعْ لِقَوْلِهِمْ كَأَنَّهُمْ خُشُبٌ مُّسَنَّدَةٌ يَحْسِبُونَ كُلَّ صَيْحَةٍ
عَلَيْهِمْ هُمُ ٱلْعَدُوُّ فَٱحْذَرْهُمْ قَٰتَلَهُمُ ٱللَّهُ أَنَّىٰ يُؤْفَكُونَ ﴿4﴾

(WAJABCIN KULAWA DA SALLAR JUMA'A)

9. Ya wadanda suka bada gaskiya! idan akayi kira ga Salla a cikin ranar Juma'a, to ku zarce izuwa sallar Juma'a, ku bar saye da sayarwa, wannan shi yafi alheri a gareku in kun kasance kun sanshi yafi amfani to ku aikata shi.

(SUFAYE SUN ƊAUKI UMARNINE NA WAZIFOFINSU DA MI'ADI DAGA WANNAN AYA)

10. Idan an gama salla to ku ɗaiɗaitu a cikin ƙasa, ku nemi arziki daga falalar Allah, ku ambaci Allah anbato maiyawa donku rabauto.(Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama ya kasance yana Huɗuba ranar Juma'a, sai ayari sukazo sai aka buga tambari saboda ayarin nan saboda al'adar da aka saba, sai mutane suka fita daga masallaci saboda ita Sai Allah ya saukar da:) .

11. Idan sun ga ciniki, sukan tarwatse don ciniki ko wasa izuwa gareshi, sukan barka (a cikin Huɗuba) kana tsaye, (kana Huɗuba,) Cene (dasu) "abindake ga Allah (na sakamako) shine yafi ga waɗanda suka bada gaskiya, (yafi wasa yafi saye da sayarwa,) Ubangiji shine mafifici shine fiyayyen mai azurtawa" (ana cewa kowane mutum yana azurta iyalinsa ai daga arzikin Allah.)

Wannan Sura Itace Suratul Munafikuna
A Madina aka saukar da ita aya goma sha ɗayace (11).
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Ita. Wannan Sura Ta ƙunshi Anbaton Munafikai Da Ayyukansu Da Siffofinsu Sannan Da Muhimman Shiryace-Shiryace Ga Muminai Ta ƙunshi Bada Labari Da ƙaurar Ma'aiki Sallallahu alaihi wa Sallama Saboda Itace Sura Ta 63 Wanda shine Adadin Shekarunsa Sallallahu alaihi WaSallama - Sawi Yayi Isharar Haka.

(ALMUNAFIKUNA)

1. Idan munafikai sunzo maka, sukan faɗa da harasansu (saɓanin abinda yake cikin zukatansu) mun shaida haƙiƙa kai ma'aikin Allah ne, Allah (Subhanahu wata'ala) yasan lallai kai ma'aikinsa ne, kuma yasan haƙiƙa munafikai maƙaryata ne (cikin abinda suka ɓoye shi, saɓanin abinda suka faɗa.)
2. Sun riƙi rantse-rantsensu garkuwa, (wato kariya a kan dukiyoyinsu da gidajensu) suka tare saboda ita ga buran hanyar Allah(wato suka hana a yaƙesu,) haƙiƙa su abinda suke aikatawa ya mugusta.
3. Wancanenka mummunan aikin nan, saboda cewasu sun bada gaskiya ne da harshe, sannan suka kafirta a zuci, (wato suka zarce a kan kafircewarsu dashi,) sai aka yimƙe a kan zukatansu da kafirci, to su basa fahimtar imani.
4. Idan ka gansu jikkunansu zasu baka mamaki (saboda kyansu, in zasuyi magana zaka saurar maganarsu (saboda girman jikkunansu da rashin fahinta,) ginshiƙaine ababan jinginawa izuwa garu, suna zaton kowace tsawa da aka aiwatar da ita, (kamar kira a sansanin yaƙi da cigiyar batacce,) araduce a kansu (saboda abinda yake cikin ƙirazansu na daga firgita, kadai abinda zai halatta jininsu yasauka,) sune ainihin magauta, to kaji tsoronsu (saboda su suna ɗaiɗaita asirinka ga kafirai) Allah ya halakar dasu, yaya suke juyawa (ga buran dalili bayan tsawon burhani?)

وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ تَعَالَوْاْ يَسْتَغْفِرْ لَكُمْ رَسُولُ اللَّهِ لَوَّوْاْ رُءُوسَهُمْ
وَرَأَيْتَهُمْ يَصُدُّونَ وَهُم مُّسْتَكْبِرُونَ ۝٥ سَوَآءٌ عَلَيْهِمْ
أَسْتَغْفَرْتَ لَهُمْ أَمْ لَمْ تَسْتَغْفِرْ لَهُمْ لَن يَغْفِرَ اللَّهُ لَهُمْ
إِنَّ اللَّهَ لَا يَهْدِي الْقَوْمَ الْفَاسِقِينَ ۝٦ هُمُ الَّذِينَ
يَقُولُونَ لَا تُنفِقُواْ عَلَىٰ مَنْ عِندَ رَسُولِ اللَّهِ حَتَّىٰ يَنفَضُّواْ
وَلِلَّهِ خَزَآئِنُ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَلَٰكِنَّ الْمُنَٰفِقِينَ
لَا يَفْقَهُونَ ۝٧ يَقُولُونَ لَئِن رَّجَعْنَا إِلَى الْمَدِينَةِ لَيُخْرِجَنَّ
الْأَعَزُّ مِنْهَا الْأَذَلَّ وَلِلَّهِ الْعِزَّةُ وَلِرَسُولِهِۦ وَلِلْمُؤْمِنِينَ
وَلَٰكِنَّ الْمُنَٰفِقِينَ لَا يَعْلَمُونَ ۝٨ * يَٰٓأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُواْ
لَا تُلْهِكُمْ أَمْوَٰلُكُمْ وَلَا أَوْلَٰدُكُمْ عَن ذِكْرِ اللَّهِ
وَمَن يَفْعَلْ ذَٰلِكَ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ الْخَٰسِرُونَ ۝٩
وَأَنفِقُواْ مِن مَّا رَزَقْنَٰكُم مِّن قَبْلِ أَن يَأْتِيَ أَحَدَكُمُ الْمَوْتُ
فَيَقُولَ رَبِّ لَوْلَا أَخَّرْتَنِي إِلَىٰ أَجَلٍ قَرِيبٍ فَأَصَّدَّقَ
وَأَكُن مِّنَ الصَّٰلِحِينَ ۝١٠ وَلَن يُؤَخِّرَ اللَّهُ نَفْسًا
إِذَا جَآءَ أَجَلُهَا وَاللَّهُ خَبِيرٌ بِمَا تَعْمَلُونَ ۝١١

ربع

5. Idan Ance dasu "Kuzo kuyi hanzari manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama ya neme maku gafara" sai sukan juyarda wuyansu, ka kan gansu suna bijirewa ga buran wannan, suna masu girmankai.
6. Daidaine garesu ka nema musu gafara ko baka nema musu gafara ba Allah bazaiyi musu gafara ba har abada, haƙiƙa Allah bazai shiryi mutane fasiƙai ba.
7. Sune waɗanda suke cewa (ga abokansu na Ansaru) kadaku ,ciyar bisa wanda yake gurin ma'aikin Allah (Sallallahu alaihi wasallama na Muhajirai) harsu tarwatse, taskokin sammai da ƙassai ko na Allah ne kaɗai, (shine mai azurta Muhajirai da waninsu,) sai dai munafukai basu fahimci haka ba.
8. Suna cewa "Wallahi idan muka koma (daga yaƙin Banil Musdaliƙi) izuwa Madina, lallai mafi girma (wato kawukansu) zai fidda mafi wulaƙanci daga gareta (wato muminai,) rinjaye kuwa na Allah ne shi kaɗai, kuma na ma'aikin Allah ne (Sallallahu alaihi wasallama) da muminai su kaɗai, sai dai munafukai basu san (haka) ba.

(FALALAR SALLA DA ANBATON ALLAH DA CIYARWA SABODA ALLAH)

9. Yaku waɗanda suka bada gaskiya! kada dukiyoyinku da ya'yanku su shagaltar daku ,ga buran anbaton Allah (kamar Salla da Hajji da Zakka, da karatun Alƙur'ani. Wanda ya aikata wancanenka haƙiƙa sune ainihin taɓaɓɓu (Sawi).
10. Kuciyar daga abinda muka azurka muku (na dukiyako ilimi wato arzuka na zahiri ko na baɗini,) tun gaban mutuwa bata zowa ɗayanku ba, ya fara cewa"Ubangijina! donme baka jinkirtamin ba izuwa ajali makusanci, inyi sadaka (da zakka da ilimi mai amfani da talifi koda karantarwa) in kasance daga salihai.
11. Allah bazai jinkirtawa wata rai idan ajalinta yazo ba, Ubangiji masanine da abinda kuke aikatawa (zai muku sakamako.)

سورة التغابن مدنية 64
وهي ثماني عشرة آية 18

بسم الله الرحمن الرحيم

يسبح لله ما في السماوات وما في الأرض له الملك وله الحمد
وهو على كل شيء قدير (1) هو الذي خلقكم
فمنكم كافر ومنكم مؤمن والله بما تعملون بصير (2)
خلق السماوات والأرض بالحق وصوركم فأحسن صوركم
وإليه المصير (3) يعلم ما في السماوات والأرض ويعلم ما تسرون
وما تعلنون والله عليم بذات الصدور (4) ألم يأتكم نبؤا الذين كفروا
من قبل فذاقوا وبال أمرهم ولهم عذاب أليم (5) ذلك بأنه
كانت تأتيهم رسلهم بالبينات فقالوا أبشر يهدوننا
فكفروا وتولوا واستغنى الله والله غني حميد (6)
ثمن
* زعم الذين كفروا أن لن يبعثوا قل بلى وربي
لتبعثن ثم لتنبؤن بما عملتم وذلك على الله يسير (7) فآمنوا
بالله ورسوله والنور الذي أنزلنا والله بما تعملون خبير (8)

Wannan Sura Itace Suratul Tagabuni

A Madina aka saukar da ita aya goma sha takwas ce (18).
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Mumunai a Lahira a keɓe.

Wannan Sura ta ƙunshi bayanin ikon Allah da Iliminsa a keɓe.

(WANI ABU DAGA MABAYYANAR KUDURARSA DA ILIMINSA)

1. Abinda yake cikin sammai da ƙassai yana tsarkakewar Ubangiji, ƙarfin sarauta naga Ubangiji da dukkan abin godewa. Shi mai ikone bisa komai.
2. Shine wanda ya halicceku, to akwai kafiri daga cikinku akwai mumini daga cikinku, (a cikin asalin halita,) sannan zai matar dasu a kan haka ya tashesu a kan haka, Ubangiji masanine da abinda kuke aikatawa.
3. Ya halicci sammai da ƙassai da gaskiya (badon wasa ba,) ya surantaku ya kyautata surorinku, (don yasanya siffar ɗan Adam mafi kyan siffofi) izuwa gareshi komai zai koma.
4. Yasan abinda yake cikin sammai da ƙassai yasan abinda kuke ɓoyewa da abinda kuke bayyanawa, Allah masanine da halin zukatan bayi da abinda yake cikinta na asirai da kudure-Kudure.

(TABBATAR DA TASHIN ALƘIYAMA DA FIRGITA KAFIRAI)

5. Shin babbar maganar waɗanda suka kafirta tun gaba baizo maka bane, na waɗanda suka kafirta tun gaba suka ɗanɗani kuɗarsu, wato uƙubar kafircinsu a duniya? Azaba mai raɗaɗi ta tabbata garesu a ranar Lahira.
6. Wancanenka azabar duniya, saboda haƙiƙa lamarin manzanninsu sun kasance sunazo musu da hujjoji mabayyana (a kan imani) sai sukace "shin bil Adama ne zasu shiryemu"? Sai suka kafi'rce suka juya baya ga buran imani, Allah ya wadata ga buran imaninsu. Ubangiji mawadacine (ga buran halitarsa,) abin godewa ne (cikin aikinsa.)
7. Waɗanda suka kafirta sun riyacewa su baza a tashesu ba, Cene (dasu) "kaina rantse da Ubangijina lallai ku za a tasheku, sannan lallai a saka muku da abinda kuka aikata, wancanenka, mai sauƙine bisa Allah."
8. To ku bada gaskiya da Allah da manzonsa, da Alƙur'ani wanda muka saukar, Allah masanine da abinda kuke aikatawa.

يَوْمَ يَجْمَعُكُمْ لِيَوْمِ الْجَمْعِ ذَٰلِكَ يَوْمُ التَّغَابُنِ وَمَنْ يُّؤْمِنْ بِاللَّهِ
وَيَعْمَلْ صَالِحاً نُّكَفِّرْ عَنْهُ سَيِّئَاتِهِ وَنُدْخِلْهُ جَنَّاتٍ تَجْرِي
مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَارُ خَالِدِينَ فِيهَا أَبَداً ذَٰلِكَ الْفَوْزُ الْعَظِيمُ ﴿9﴾
وَالَّذِينَ كَفَرُوا وَكَذَّبُوا بِآيَاتِنَا أُولَٰئِكَ أَصْحَابُ النَّارِ
خَالِدِينَ فِيهَا وَبِئْسَ الْمَصِيرُ ﴿10﴾ مَا أَصَابَ مِن مُّصِيبَةٍ
إِلَّا بِإِذْنِ اللَّهِ وَمَنْ يُّؤْمِنْ بِاللَّهِ يَهْدِ قَلْبَهُ وَاللَّهُ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمٌ ﴿11﴾
وَأَطِيعُوا اللَّهَ وَأَطِيعُوا الرَّسُولَ فَإِن تَوَلَّيْتُمْ فَإِنَّمَا عَلَىٰ رَسُولِنَا
الْبَلَاغُ الْمُبِينُ ﴿12﴾ اللَّهُ لَا إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَعَلَى اللَّهِ فَلْيَتَوَكَّلِ
الْمُؤْمِنُونَ ﴿13﴾ * يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا إِنَّ مِنْ أَزْوَاجِكُمْ
وَأَوْلَادِكُمْ عَدُوّاً لَّكُمْ فَاحْذَرُوهُمْ وَإِن تَعْفُوا
وَتَصْفَحُوا وَتَغْفِرُوا فَإِنَّ اللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿14﴾ إِنَّمَا أَمْوَالُكُمْ
وَأَوْلَادُكُمْ فِتْنَةٌ وَاللَّهُ عِندَهُ أَجْرٌ عَظِيمٌ ﴿15﴾ فَاتَّقُوا اللَّهَ مَا اسْتَطَعْتُمْ
وَاسْمَعُوا وَأَطِيعُوا وَأَنفِقُوا خَيْراً لِّأَنفُسِكُمْ وَمَنْ يُّوقَ شُحَّ نَفْسِهِ
فَأُولَٰئِكَ هُمُ الْمُفْلِحُونَ ﴿16﴾ إِن تُقْرِضُوا اللَّهَ قَرْضاً حَسَناً يُضَٰعِفْهُ لَكُمْ
وَيَغْفِرْ لَكُمْ وَاللَّهُ شَكُورٌ حَلِيمٌ ﴿17﴾ عَالِمُ الْغَيْبِ وَالشَّهَادَةِ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ ﴿18﴾

ربع

9. Anbaci ranar da yake taraku a cikin taron Alƙiyama, wancanenka shine ranar kamunga (da muminai za suyiwa kafirai kamunga da karɓar gidaddajinsu da iyalinsu a gidan Aljanna,) wanda ya bada gaskiya da Allah yayi aiki na gari zai kankare miyagun ayyuka ga buransa, zai shigar dashi cikin aljannatai, wacce ƙoramu take kwarara ƙarƙashinta, masu dauwama a cikinta har abada, wancanenka shine rabo mai girma.
10. Waɗanda suka kafirta suka ƙaryata da ayoyinmu (Alƙur'ani) waɗancanenka sune yan wuta masu dauwama a cikinta, tur makoma ita wuta!
11. Babu wata musiba da zata samu wani mutum saida izinin Allah, wanda ya bada gaskiya da Allah (a cikin faɗinsa cewa musiba saida izinin Allah,) zai shiryi zuciyarsa (da haƙuri a kanta,) Allah masanine da komai.
12. Kubi Allah kubi ma'aikinsa(Sallallahu alaihi wasallama,) to in kuka bada baya, to dahir iyar da saƙo mabayyani shine a kan manzonmu.
13. Allah babu abin bautawa da gaskiya saishi, a bisa ga Allah duka muminai suka dogara.

(WA'AZI DA IRSHADI-SHIRYARWA)

14. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya! haƙiƙa akwai magauta gareku a cikin matayenku da ya'yenku, to kuji tsoronsu, (kadaku ,bisu a cikin jinkiri ga buran alheri, kamar yaƙi da hijira, saboda sababin saukar wannan aya ya kasance a cikin bin'ya'ya da mata saboda sun nufi suyi hijira tareda ma'aiki Sallallahu alaihi wasallama matansu da 'ya'yayensu suka hanasu, haka kuma Awfu ɗan Maliku al-Ashja'iy, yana da 'ya'yaye yanufi zai fita yaƙi suka ɓarke masa da kuka, sukace "izuwa wa zaka barmu" sai yaji tausayinsu yayi zamansa bai fita yaƙi ba) In kukayi rangwame ga buransu, (wato kuka bar uƙubarsu da barin ciyarwa a garesu, kukayi rangwame a cikin sanyayar da gwiwar da sukayi muku a cikin wancanenka alheri, kuna masu kafa dalili da tausayin rabuwarku a kansu) kukayi gafara, haƙiƙa Ubangiji mai gafara ne mai jinƙai.
15. Dahir da dukiyoyinku da'ya'yanku fitina ne kawai, (masu shagalar daku ,ga buran ayyukan lahira) lada mai girma yana ga Ubangiji, (kadaku ,kore ladan da shagalarku da dukiyoyi da 'ya'yaye.)
16. To kuji tsoron Allah gwargwadon ikonku, (ta shafe faɗin kuji tsoron Allah yadda ya kamata aji tsoronsa,) kuji abinda aka umarceku dashi jin karɓa, kubi kuciyar a cikin ɗa'ar Allah zaifi alheri ga kawukanku, duk wanda aka kiyashe shi son kansa to haƙiƙa wancanenka sune marabauta.
17. In kun rantawa Allah rance mai kyau, to kukayi sadaka ga daɗin ranku, zai ninninka muku (izuwa ɗari bakwai ko fiye,) zai gafarta muku (abinda yaga dama,) Allah mai babban sakamako ne (a kan aiki,) mai jinkirin azabane (ga mai saɓo).
18.Masanin asirin fake dana sarari, mabuwayi (cikin mulkinsa) gwani (cikin aikinsa).

65 سُورَةُ الطَّلَاقِ مَدَنِيَّةٌ

وَهِيَ اثْنَتَا عَشْرَةَ ءَايَةً 12

بِسْمِ اِ۬للَّهِ اِ۬لرَّحْمَٰنِ اِ۬لرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا اَ۬لنَّبِٓيٓءُ إِذَا طَلَّقْتُمُ اُ۬لنِّسَآءَ فَطَلِّقُوهُنَّ لِعِدَّتِهِنَّ
وَأَحْصُواْ اُ۬لْعِدَّةَۖ وَاتَّقُواْ اُ۬للَّهَ رَبَّكُمْۖ لَا تُخْرِجُوهُنَّ مِنۢ بُيُوتِهِنَّ
وَلَا يَخْرُجْنَ إِلَّآ أَن يَأْتِينَ بِفَٰحِشَةٖ مُّبَيِّنَةٖۖ وَتِلْكَ حُدُودُ اُ۬للَّهِۖ
وَمَن يَتَعَدَّ حُدُودَ اَ۬للَّهِ فَقَدْ ظَلَمَ نَفْسَهُۥۖ لَا تَدْرِے لَعَلَّ اَ۬للَّهَ
يُحْدِثُ بَعْدَ ذَٰلِكَ أَمْراٗۖ (1) فَإِذَا بَلَغْنَ أَجَلَهُنَّ فَأَمْسِكُوهُنَّ
بِمَعْرُوفٍ أَوْ فَارِقُوهُنَّ بِمَعْرُوفٖۖ وَأَشْهِدُواْ ذَوَےْ عَدْلٖ مِّنكُمْ
وَأَقِيمُواْ اُ۬لشَّهَٰدَةَ لِلَّهِۖ ذَٰلِكُمْ يُوعَظُ بِهِۦ مَن كَانَ يُؤْمِنُ بِاللَّهِ
وَالْيَوْمِ اِ۬لْأٓخِرِۖ وَمَن يَتَّقِ اِ۬للَّهَ يَجْعَل لَّهُۥ مَخْرَجاٗ وَيَرْزُقْهُ مِنْ
حَيْثُ لَا يَحْتَسِبُۖ وَمَن يَتَوَكَّلْ عَلَى اَ۬للَّهِ فَهْوَ حَسْبُهُۥٓۖ إِنَّ اَ۬للَّهَ
بَٰلِغُ أَمْرِهِۦۖ قَدْ جَعَلَ اَ۬للَّهُ لِكُلِّ شَےْءٖ قَدْراٗۖ (2) وَالَّٰٓـِٔ يَئِسْنَ
مِنَ اَ۬لْمَحِيضِ مِن نِّسَآئِكُمْ إِنِ اِ۪رْتَبْتُمْ فَعِدَّتُهُنَّ ثَلَٰثَةُ أَشْهُرٖ وَالَّٰٓـِٔ لَمْ يَحِضْنَۖ
وَأُوْلَٰتُ اُ۬لْأَحْمَالِ أَجَلُهُنَّ أَن يَضَعْنَ حَمْلَهُنَّۖ وَمَن يَتَّقِ اِ۬للَّهَ يَجْعَل لَّهُۥ مِنْ أَمْرِهِۦ يُسْراٗۖ (3)

Wannan Sura Itace Suratul Ɗalaƙi

A Madina aka saukar da ita aya goma sha biyuce (12).
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

Wannan Sura ta tattara bisa hukunce-hukuncen idda da ban tsoro da aƙibar masu saɓawa Allah da firgitarwa.)

(HUKUNCE-HUKUNCE DATA RATAYA DA IDDA)

1.Ya wannan Annabi (mai girma, ana nufin al'ummarsa) in kun nufin sakin mata, (ba ace in kayi nufin sakin mata, saboda ban girma,) to ku sakésu da farkon iddarsu, (shine ya kasance a cikin tsarki da ba a kusaceta ba a cikinsa saboda Annabi Sallallahu alaihi wasallama ya fassara shi da wannan Shaihani sun ruwaito shi,) Ku kiyaye iddar nan (don kuyi kome tun gaban ƙarewarta,) kuji tsoron Allah Ubangijinku (kubishi cikin umarninsa da haninsa,) karku fishshe su daga ɗakunansu kadasu kuma su fita daga ita har iddarsu ta ƙare, sai dai in sunzo da zina mabayyaniya (to a fishshe su don a tsaida haddi kansu,) wadancanenka ababan ambato iyakokin Allah ne duka wanda ya ƙetare iyakokin Allah, to haƙiƙa ya zalunci kansa, baka sani ba, watakila Ubangiji ya farar da wani al'amari bayan wancanenka (shika shine kome idan shikan ta kasance ɗayace ko biyu.)

(TAKAWA TANA DAGA MANYAN SABUBBAN ARZIKI)

2. In suka kusanci ƙarewar iddarsu to ku koma dasu da abin sani ba tareda cuta ba, koku rabu dasu da abin sani, ku barsu har iddarsu ta ƙare, karku cucesu da kome, ku shaidar da ma'abota adalci daga cikinku bisa kome ko rabuwa ku tsaida shaida don Allah (badon wanda za ayiwa shaida ba, mummuna gareshi ko kyakykyawa,) wancanenku ana wa'azi dashi ga wanda ya kasance, ya bada gaskiya da ranar Lahira, wanda yaji tsoron Allah yasanya masa yayewa.
3. Ya azurtashi ta inda baya zato. Duk wanda ya dogara da Allah Allah ne ma'ishinsa, Ubangiji mai isa al'amarinsa ne, haƙiƙa Ubangiji yasanya lokaci ga kowane abu.

ذَٰلِكَ أَمْرُ اللَّهِ أَنزَلَهُۥٓ إِلَيْكُمْ وَمَنْ يَّتَّقِ اللَّهَ يُكَفِّرْ عَنْهُ سَيِّـَٔاتِهِۦ وَيُعْظِمْ لَهُۥٓ
أَجْراً ﴿4﴾ ۞ أَسْكِنُوهُنَّ مِنْ حَيْثُ سَكَنتُم مِّن وُجْدِكُمْ وَلَا تُضَآرُّوهُنَّ لِتُضَيِّقُواْ ثمن
عَلَيْهِنَّ وَإِن كُنَّ أُوْلَٰتِ حَمْلٍ فَأَنفِقُواْ عَلَيْهِنَّ حَتَّىٰ يَضَعْنَ حَمْلَهُنَّ
فَإِنْ أَرْضَعْنَ لَكُمْ فَـَٔاتُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ وَأْتَمِرُواْ بَيْنَكُم بِمَعْرُوفٍ وَإِن تَعَاسَرْتُمْ
فَسَتُرْضِعُ لَهُۥٓ أُخْرَىٰ ﴿5﴾ لِيُنفِقْ ذُو سَعَةٍ مِّن سَعَتِهِۦ وَمَن قُدِرَ عَلَيْهِ رِزْقُهُۥ
فَلْيُنفِقْ مِمَّآ ءَاتَىٰهُ اللَّهُ لَا يُكَلِّفُ اللَّهُ نَفْساً إِلَّا مَآ ءَاتَىٰهَا
سَيَجْعَلُ اللَّهُ بَعْدَ عُسْرٍ يُسْراً ﴿6﴾ وَكَأَيِّن مِّن قَرْيَةٍ عَتَتْ عَنْ
أَمْرِ رَبِّهَا وَرُسُلِهِۦ فَحَاسَبْنَٰهَا حِسَاباً شَدِيداً وَعَذَّبْنَٰهَا عَذَاباً نُّكْراً ﴿7﴾
فَذَاقَتْ وَبَالَ أَمْرِهَا وَكَانَ عَٰقِبَةُ أَمْرِهَا خُسْراً ﴿8﴾ أَعَدَّ اللَّهُ لَهُمْ
عَذَاباً شَدِيداً فَاتَّقُواْ اللَّهَ يَٰٓأُوْلِي الْأَلْبَٰبِ ﴿9﴾ الَّذِينَ ءَامَنُواْ قَدْ أَنزَلَ اللَّهُ
إِلَيْكُمْ ذِكْراً ﴿10﴾ رَّسُولاً يَتْلُواْ عَلَيْكُمْ ءَايَٰتِ اللَّهِ مُبَيِّنَٰتٍ لِّيُخْرِجَ الَّذِينَ ءَامَنُواْ
وَعَمِلُواْ الصَّٰلِحَٰتِ مِنَ الظُّلُمَٰتِ إِلَى النُّورِ وَمَن يُؤْمِنۢ بِاللَّهِ وَيَعْمَلْ صَٰلِحاً نُّدْخِلْهُ
جَنَّٰتٍ تَجْرِي مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَداً قَدْ أَحْسَنَ اللَّهُ لَهُۥ رِزْقاً ﴿11﴾
۞ اللَّهُ الَّذِي خَلَقَ سَبْعَ سَمَٰوَٰتٍ وَمِنَ الْأَرْضِ مِثْلَهُنَّ يَتَنَزَّلُ الْأَمْرُ بَيْنَهُنَّ ربع
لِتَعْلَمُواْ أَنَّ اللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ وَأَنَّ اللَّهَ قَدْ أَحَاطَ بِكُلِّ شَيْءٍ عِلْماً ﴿12﴾

(FA'IDODIN TAƘAWA)

4. Waɗannan da suka ɗebe haso daga haila daga matayenku in kukayi tababa a cikin iddarsu, to iddarsu wata ukune, waɗanda basa yin haila (saboda ƙanƙantarsu to iddarsu wata uku, mas'alan nan guda biyu a cikin waɗansun da mazansu suka mutune ammasu iddarsu za suyi sauraro wata huɗu da kwana goma,) ma'abota ciki kuma, ƙarewar iddarsu, (sakinsu akayi ko mazajensune suka mutu,) su haife cikinsu, wanda, yake jin tsoron Allah zai sanya masa sauƙi daga lamarinsa (a duniya da Lahira.)
5. Wancanenka hukunci cikin idda, hukuncin Allah ne ya saukar dashi, wanda yaji tsoron Allah ya kankare masa miyagun ayyukansa, zai girmama lada gareshi.
6. Ku zaunar dasu (ababan saki) ta inda kuka zauna na daga gwargwadon ƙarfinku, kada kucuci matanku donku ƙuntata (ɗakuna) a garesu (su buƙata izuwa fita, ko izuwa abinci, suyi fansa daga gareku) in sun kasance ma'abota ciki, to kuciyar a garesu harsu haife cikinsu, to insun shayar muku da ya'yanku (waɗanda suka haifa muku), to ku basu ladan shayarwarsu, kubi umarni na Allah tsakaninku dasu da kyakkyawa a shari'a a cikin haƙƙin 'ya'yayen, (shine ku tsaya a kan lada abin sani shine shayarwa, in kun ƙuntata (shayarwa uba bai bada lada ba, uwa kuma taƙi shayarwa) to wata ta shayar ga uban nan, baza a tilashi uwa bisa shayar dashi ba.
7. Ma'abucin yalwa ya ciyar daga yalwarsa, wanda aka ƙuntata arzikinsu to ya ciyar daga abinda Allah ya bashi gwargwadon ikonsa, Allah baya kallafawa mutum sai gwargwadon ikon daya bashi, da sannu Allah zai sanya sauƙi bayan tsanani.
8. Da yawa na daga alƙaryu da mutanenta sukayi girmankai da al'amarin Ubangiji da manzannin Ubangiji, to mukayi mata hisabi a Lahira koda yake batazo ba, don an tabbata za tazone, hisabi mai tsanani mukayi mata azaba, azaba mai ƙarni (azabar wuta.) Kuji tsoron Allah ya ma'abota hankula waɗanda suka bada gaskiya.
9. Ta ɗanɗani kuɗarta, aƙibar al'amarinta ya zama taɓewa.
10. Ubangiji ya tanadi azaba mai tsanani garesu, kuji tsoron Allah yaku ma'abota hankula, waɗanda suka bada gaskiya, allah ya saukar da ɗaukaka gareku (Shine Alƙur'ani).
11. Ya aiko manzo (Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama) da yake karantawan ayoyin Allah gareku mabayyana don yafitar da waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru (bayan zuwan Alƙur'ani da manzo,) ya fishshesu daga duffan kafirci izuwa haske (Shine imani,) wanda ya bada gaskiya da Allah yayi aiki na gari zai shigar dashi aljannatai wacce ƙoramu take kwarara ƙarƙashinta masu dauwama a cikinta har abada, haƙiƙa Allah ya kyautata arziki gareshi (Shine arzikin Aljanna wacce ni'imarta bazata yanke ba.)
12. Allah Shine ya halicci sammai bakwai da ƙassai misalinsu (guda bakwai,) wahayi na sauka tsakaninsu, (Jibrilu yana sauka dashi daga sama ta bakwai izuwa ƙasa ta bakwai), haƙiƙa Allah mai ikone bisa komai, haƙiƙa ilimin Ubangiji ya kewaye da kowane abu.

66 سُورَةُ التَّحْرِيمِ مَدَنِيَّة

وهي اثنتا عشرة ءاية 12

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيٓءُ لِمَ تُحَرِّمُ مَآ أَحَلَّ ٱللَّهُ لَكَ تَبْتَغِي مَرْضَاتَ أَزْوَٰجِكَ وَٱللَّهُ
غَفُورٞ رَّحِيمٞ ﴿1﴾ قَدْ فَرَضَ ٱللَّهُ لَكُمْ تَحِلَّةَ أَيْمَٰنِكُمْ وَٱللَّهُ مَوْلَىٰكُمْ وَهُوَ
ٱلْعَلِيمُ ٱلْحَكِيمُ ﴿2﴾ وَإِذْ أَسَرَّ ٱلنَّبِيٓءُ إِلَىٰ بَعْضِ أَزْوَٰجِهِۦ حَدِيثاً فَلَمَّا
نَبَّأَتْ بِهِۦ وَأَظْهَرَهُ ٱللَّهُ عَلَيْهِ عَرَفَ بَعْضَهُۥ وَأَعْرَضَ عَنۢ بَعْضٍ فَلَمَّا نَبَّأَهَا بِهِۦ
قَالَتْ مَنْ أَنۢبَأَكَ هَٰذَا قَالَ نَبَّأَنِيَ ٱلْعَلِيمُ ٱلْخَبِيرُ ﴿3﴾ إِن تَتُوبَآ إِلَى ٱللَّهِ
فَقَدْ صَغَتْ قُلُوبُكُمَا وَإِن تَظَّٰهَرَا عَلَيْهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ هُوَ مَوْلَىٰهُ وَجِبْرِيلُ
وَصَٰلِحُ ٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ بَعْدَ ذَٰلِكَ ظَهِيرٌ ﴿4﴾ عَسَىٰ رَبُّهُۥٓ إِن طَلَّقَكُنَّ
أَن يُبْدِلَهُۥٓ أَزْوَٰجاً خَيْراً مِّنكُنَّ مُسْلِمَٰتٖ مُّؤْمِنَٰتٖ قَٰنِتَٰتٖ تَٰٓئِبَٰتٍ
عَٰبِدَٰتٖ سَٰٓئِحَٰتٖ ثَيِّبَٰتٖ وَأَبْكَاراً ﴿5﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قُوٓاْ أَنفُسَكُمْ
وَأَهْلِيكُمْ نَاراً وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ وَٱلْحِجَارَةُ عَلَيْهَا مَلَٰٓئِكَةٌ غِلَاظٞ شِدَادٞ
لَّا يَعْصُونَ ٱللَّهَ مَآ أَمَرَهُمْ وَيَفْعَلُونَ مَا يُؤْمَرُونَ ﴿6﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ لَا تَعْتَذِرُواْ ٱلْيَوْمَ إِنَّمَا تُجْزَوْنَ مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿7﴾

Wannan Sura Itace Suratul Taharimi
A Madina aka saukar da ita aya goma sha biyuce (12)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

Wannan sura ta ƙunshi husumar matan Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama da ba'alin abinda ya faru daga matayensa da waɗansu wa'aze-wa'aze da tarbiyoyi da sanya misalce-misalce.

(GIRMAMA MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA DAYA ZARGESHI DA WAHALAR DA KANSA A KAN YARDA DA ZARGIN MATAYENSA)

1. Ya wannan Annabi (mai girma) donme kake harantawar abinda Allah ya halattashi gareka (wannan zance yana ƙunshe ne da matuƙar girmamawa ga Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama yayin daya zargeshi a kan ƙuntatawa kansa saboda neman yardar matayensa. Kamar Ubangiji Subhanahu wata'ala yana cewa, kadaka wahalar da kanka a cikin neman yardar matayen aurenka, hutar da kanka karka wahalar da ita,) donme kake haramtawar abinda Allah ya halatta maka (wato Mariyatul kibɗiyya yayin daya sadu da ita a ɗakin Nana Hafsatu a halin batanan, to saita zo, wato zaman wannan abu a ɗakinta ya dameta, kuma a shimfiɗarta, lokacin da kace "ita haramun ce gareka",) kana neman yardar matayen aurenka da haramta ta a kanka, Allah mai gafarar haramtawar ne gareka mai rahama.
2. Ubangiji ya shar'anta maka wargazawar rantsuwarka, (Ya wajabta muku yin haka da kaffara a cikin suratul Ma'ida, haramta kuyanga yana daga rantse-rantsen, shin Annabi Sallallahu alaihi wasallama yayi kaffara? Muƙatilu yace 'ya'yanta wuyaye, a cikin haramta Mariyatu, Alhasan yace baiyi ba,) Allah ne mataimakinku, Allah Shine masani mai hikima.
3. Ka ambata zamanin da Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) ya asirta magana (ga Nana Hafsatu Raliyallahu anha Shine haramta Mariyatu, yace da ita "kadaki ɗaiɗaita wannan labarin",) yayin data tseguntawa (Nana A'ishatu) dashi, (tana zaton ba laifi a cikin wancanenka,) Allah ya tsinkayar dashi a kan wannan abin tseguntawa, sai yasanar da shashinsa (ga Nana Hafsatu), ya bijire ga buran shashin, (don karamci daga gareshi,) to zamanin daya bata labari dashi, saitace "waya baka wannan labari?" yace "Allah masanin asirin fakenc ya bani wannan labari."
4. Inkun tuba izuwa Allah (a karɓeku) haƙiƙa zukatanku sun karkata, (izuwa haramcin Mariyatu Raliyallahu anha, wato wannan ya faranta muku, tareda ƙin Annabi Sallallahu alaihi wasallama ga wancanenku ko zunubi ne,) inkun gama kanku ga Annabi (Sallallahu alaihi wasallama cikin abinda yake ƙi) to haƙiƙa Allah Shine mataimakinsa da Jibrilu da salihan muminai, (Abubakar da Umaru Allah ya ƙara yarda a garesu.) Mala'iku bayan wancanenka mataimaka ne a gareshi.
5. Ana ƙaunar Ubangijinsa inya sakeku ya misanya masa matan aure da suka fiku, Musulmai, Muminai masu biyayya, masu tuba ga Allah masu bauta ga Allah, masu Azumi zawarawa da 'yan mata.

(FUSKANCE-FUSKANCE DA GARGAƊE-GARGAƊE)

6. Yaku waɗanda kuka bada gaskiya! Ku kiyaye kawukankuda iyalinku daga shiga wuta wacce gumagumanta kafirai da duwarwatsu (kamar gumakansu na duwarwatsu, yana nufin cewa haƙiƙa wuta mai yawan zafice, tana huruwa da abinda aka ambata, ba kamar wutar duniya wacce take huruwa da Itace da waninsa ba,) Mala'iku (goma sha tara) suna tsaronta, masu kaurin zuciya masu ƙarfin riƙo, basa saɓawa Allah abinda ya umarcesu (suna aika duk abinda ya umarcesu, ban tsorone ga muminai gameda yin ridda,hakanan kuma munafikai masu bada gaskiya da harshe ba a zuci ba.)
7. Yaku waɗanda kuka kafirta! kar kuyi hanzari a yau, (ana faɗa musu wannanne yayin shigarsu wuta domin hanzarin bazai amfaneku ba,) dahir dai ana saka muku abinda kuka kasance kuna aikatawa.

ثمن

* يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ تُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ تَوْبَةٗ نَّصُوحًا عَسَىٰ رَبُّكُمْ
أَن يُكَفِّرَ عَنكُمْ سَيِّـَٔاتِكُمْ وَيُدْخِلَكُمْ جَنَّٰتٖ تَجْرِي مِن
تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ يَوْمَ لَا يُخْزِي ٱللَّهُ ٱلنَّبِيَّ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥۖ
نُورُهُمْ يَسْعَىٰ بَيْنَ أَيْدِيهِمْ وَبِأَيْمَٰنِهِمْ يَقُولُونَ رَبَّنَآ
أَتْمِمْ لَنَا نُورَنَا وَٱغْفِرْ لَنَآۖ إِنَّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٖ قَدِيرٞ ٨
يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ جَٰهِدِ ٱلْكُفَّارَ وَٱلْمُنَٰفِقِينَ وَٱغْلُظْ عَلَيْهِمْۚ وَمَأْوَىٰهُمْ
جَهَنَّمُۖ وَبِئْسَ ٱلْمَصِيرُ ٩ ضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلٗا لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ
ٱمْرَأَتَ نُوحٖ وَٱمْرَأَتَ لُوطٖۖ كَانَتَا تَحْتَ عَبْدَيْنِ مِنْ عِبَادِنَا
صَٰلِحَيْنِ فَخَانَتَاهُمَا فَلَمْ يُغْنِيَا عَنْهُمَا مِنَ ٱللَّهِ شَيْـٔٗا
وَقِيلَ ٱدْخُلَا ٱلنَّارَ مَعَ ٱلدَّٰخِلِينَ ١٠ وَضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلٗا
لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱمْرَأَتَ فِرْعَوْنَ إِذْ قَالَتْ رَبِّ
ٱبْنِ لِي عِندَكَ بَيْتٗا فِي ٱلْجَنَّةِ وَنَجِّنِي مِن فِرْعَوْنَ وَعَمَلِهِۦ
وَنَجِّنِي مِنَ ٱلْقَوْمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ١١ وَمَرْيَمَ ٱبْنَتَ عِمْرَٰنَ
ٱلَّتِيٓ أَحْصَنَتْ فَرْجَهَا فَنَفَخْنَا فِيهِ مِن رُّوحِنَا وَصَدَّقَتْ
بِكَلِمَٰتِ رَبِّهَا وَكُتُبِهِۦ وَكَانَتْ مِنَ ٱلْقَٰنِتِينَ ١٢

8. Yaku wađanda suka bada gaskiya! ku tuba izuwa Allah tuba ta gaskiya, (Shine bazaku koma izuwa zunubi ba, bazaku nufi komawa gareshi ba,) ana ƙaunar Ubangijinku ya kankare muku miyagun ayyukanku, ya shigar daku ,aljannatai wacce ƙoramu take kwarara ƙarƙashinta, ranar da Allah bazai kunyatar da Annabi (SallAllahu alaihi wasallama) ba da wađanda suka bada gaskiya tare dashi, haskensu yana tafe nan gabansu, yana kasancewa kuma a damammakinsu, suna cewa, "Ubangijinmu cika mana haskenmu (izuwa Aljanna" munafikai ko ana bice haskensu suna cewa) "Kai gafara garemu ya Ubangijinmu, haƙiƙa kai mai ikone bisa komai".

9. Ya wannan Annabi (Maigirma!) Yaƙi kafirai (da kansakali) ka yaƙi munafukai (da harshe da hujja ko kaurara garesu (da tsana,) jahannama ce makomarsu tur! makoma ita.

(MISALCE-MISALCE MUHIMMAI NA MATAYE)

10. Ubangiji ya saba misali ga wađanda suka kafirta matar Annabi Nuhu (sunanta Wahilatu) da matar Annabi Hudu (sunanta Wailatu,) sun kasance ƙarƙashin bayi biyu daga bayinmu salihai guda biyu, sai suka zambacesu (a addini ba zina ba, saboda matar Annabi bata taɓa zina ba, matar Annabi Nuhu tanace da mutanensa mahaukaci ne, matar Annabi Luđu tana shigar da mutanensa a kan baƙinsa inda daddare ne ta hura wuta, da rana kuma ta hura hayaƙi,) to (Annabi Nuhu da Annabi Luđu) basu tsare masu komai ba (na azabar lahira,) Ance dasu "Ku shiga wuta tareda masu shigar ta,"(Kafiran mutanen Annabi Nuhu da Annabi Luđu.)

11. Ubangiji yasanya misali ga wađanda suka bada gaskiya, matar Fir'auna (ta bada gaskiya da Annabi Musa sunanta Asiyatu, Fir'auna yayi mata azaba ya tirkance hannuwanta da ƙafafuwanta ya jefa dutsan niƙa mai girma a ƙirjinta, ya fuskantar da ita izuwa rana ta kasance idan mutanen da aka wakkala da ita suka kau sai Mala'iku suyimata inuwa, ta kasance tana fađa yayin da akeyi mata azaba) "Ya Ubangijina! gina min đaki a gurinka a cikin aljanna (sai aka yaye mata saita ga Aljanna sai wannan ya sauwaƙe mata ta zama bata jin azabar,) ka tserar dani daga Fir'auna da aikinsa (nazaba,) ka tserar dani daga mutane azzalumai. (Sai Allah ya karɓi ranta, Ibn kaisana yace "an đauketa da ranta aka kaita cikin aljanna tana nan tana ci tana sha a cikin al-janna.")

12. Yasanya misali na Maryamu 'Yar Imranu wacce ta kiyaye farjinta mukayi busa a cikinsa daga ran namu (wato Jibrilu, yayi busa a cikin wuyan aljihun rigarta ubangiji ya isar da aikinsa izuwa farjinta, saita sami cikin Annabi Isa, Alaihissalamu) ta gasgata shari'o'in Ubangijinta da littattafansa (ababan saukarwa) ta kasance daga masu đa'a ga Allah.

حزب

67 سورة الملك مكية
وهي ثلاثون آية 30

بسم الله الرحمن الرحيم

* تبارك الذي بيده الملك وهو على كل شيء قدير (1) الذي خلق الموت
والحياة ليبلوكم أيكم أحسن عملا وهو العزيز الغفور (2) الذي خلق سبع
سماوات طباقا ما ترى في خلق الرحمن من تفاوت فارجع البصر هل ترى
من فطور (3) ثم ارجع البصر كرتين ينقلب إليك البصر خاسئا وهو
حسير (4) ولقد زينا السماء الدنيا بمصابيح وجعلناها رجوما للشياطين
وأعتدنا لهم عذاب السعير (5) وللذين كفروا بربهم عذاب جهنم
وبئس المصير (6) إذا ألقوا فيها سمعوا لها شهيقا وهي تفور (7) تكاد
تميز من الغيظ كلما ألقي فيها فوج سألهم خزنتها ألم ياتكم نذير (8)
قالوا بلى قد جاءنا نذير فكذبنا وقلنا ما نزل الله من شيء إن أنتم
إلا في ضلال كبير (9) وقالوا لو كنا نسمع أو نعقل ما كنا في أصحاب
السعير (10) فاعترفوا بذنبهم فسحقا لأصحاب السعير (11)
إن الذين يخشون ربهم بالغيب لهم مغفرة وأجر كبير (12)

Wannan Sura Itace Suratul Maliki Azza Wa Jalla
a Makka aka saukar da ita aya talatin da ɗayace (31)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan sura ta ƙunshi tabbatar girman ƙudurar Ubangiji da Iliminsa da bayanin ni'imominsa bisa bayinsa, da abinda suke gamuwa dashi ranar Alƙiyama.

(WANI ABU DAGA)

1. Sarkin nan da mulki da ƙarfin sarauta yake hannunsa a cikin sarautarsa, alherinsa ya daɗu ya yawaita, kuma ya tsarkaka ga buran sifofin hadisai, shi mai ikone bisa komai.
2. Wanda ya halicci mutuwa (a duniya) da rayuwa (a lahira; rayuwa wato rai Itace abinda jin motsi yake tabbata da ita) donya jarrabeku (a rayuwa,) wannenenkune mafi kyan aiki ga Allah? Shine mabuwayi (a cikin uƙubarsa ga wanda ya saɓe shi,) mai gafara (ga wanda ya tuba.)
3. Wanda ya halicci sammai bakwai, wata sama a kan wata, (ba tareda shafar juna ba,) baka ganin rashin dacewa a cikin halittar da yayi musu ko yayiwa waninsu. Maida dubanka izuwa sama, ko kaga tsagewa a cikinta?
4. Sannan ka sake maida dubanka sau da yawa idonka yakomo yana taɓe, bada yaga cikasba, (wato tawaya,) alhali yana yanke (ga buran ganin cikas.)
5. Haƙiƙa mun ƙawata saman duniya makusanciya izuwa ƙasa, da taurari, mun sanya ta ɗuwarwatsun jifa na shaiɗanu, (in sun nemi satarji, Shine tauraro ya waro kamar garwashin wuta ya kashe.aljan, ba tauraron yake tahowa ba, wani abune daga cikin tauraron yake fitowa.) Mun tanadi azabar wuta abar hurawa garesu (domin tauraro baya gushewa ga buran gurinsa.)
6. Azabar jahannama ta tabbata ga waɗanda suka kafirta da Ubangijinsu, tur makoma ita!
7. In aka zubasu cikinta sai suyi kururuwa daga gareta alhali tana tafarfasa.
8. Tana' kusanta ta kyarkece, saboda fushi kan kafirai koda yaushe aka zuba jama'a cikinta daga garesu, mataskatanta saisu tambaye su, (tambayo na urustawa,) shin mai gargaɗi baizo muku bane, (dazai tsoratar daku ,azabar Allah da ita?)
9. Saisu ce "i, haƙiƙa mai gargaɗi yazo mana".
10. "Muka ƙaryata, mukace "Allah bai saukar da kome ba, ku baku kasance ba, sai a cikin ɓata mai girma." (Mala'iku suna faɗawa kafiran haka ko kuma kafirai suna faɗawa manzannin haka.)
11. Sukace "Da mun kasance munaji, (jin fahinta,) ko muna hankalta, (hankalin tunani) da bamu zamo cikin 'yan wuta ba.
12. Sukayi furuci da zunubinsu, (lokacin da furuci bazai anfane su ba) to nisa ya tabbata ga 'yan wuta (ga buran rahamar Ubangiji, ma'ana Allah ya nisanta su nisantawa.)

وَأَسِرُّواْ قَوْلَكُمُۥٓ أَوِ اِجْهَرُواْ بِهِۦٓۖ إِنَّهُۥ عَلِيمُۢ بِذَاتِ الصُّدُورِۖ 13
أَلَا يَعْلَمُ مَنْ خَلَقَ وَهْوَ اَللَّطِيفُ الْخَبِيرُۖ 14 هُوَ اَلذِے جَعَلَ لَكُمُ
اُلْأَرْضَ ذَلُولاٗ فَامْشُواْ فِے مَنَاكِبِهَا وَكُلُواْ مِن رِّزْقِهِۦۖ وَإِلَيْهِ
اِلنُّشُورُۖ 15 ءَآمِنتُم مَّن فِے السَّمَآءِ أَن يَّخْسِفَ بِكُمُ الْأَرْضَ
فَإِذَا هِيَ تَمُورُۖ 16 أَمْ اَمِنتُم مَّن فِے السَّمَآءِ أَنْ يُّرْسِلَ عَلَيْكُمْ حَاصِباٗ
فَسَتَعْلَمُونَ كَيْفَ نَذِيرِۖ 17 وَلَقَدْ كَذَّبَ اَلذِينَ مِن قَبْلِهِمْ
فَكَيْفَ كَانَ نَكِيرِۖ 18 * أَوَلَمْ يَرَوْاْ إِلَى اَلطَّيْرِ فَوْقَهُمْ صَٰٓفَّٰتٖ
وَيَقْبِضْنَۖ مَا يُمْسِكُهُنَّ إِلَّا اَلرَّحْمَٰنُۖ إِنَّهُۥ بِكُلِّ شَےْءِۢ بَصِيرٌۖ 19 أَمَّنْ هَٰذَا اَلذِے
هُوَ جُندٞ لَّكُمْ يَنصُرُكُم مِّن دُونِ اِلرَّحْمَٰنِۖ إِنِ اِلْكَٰفِرُونَ إِلَّا فِے غُرُورٍۖ 20
أَمَّنْ هَٰذَا اَلذِے يَرْزُقُكُمُۥٓ إِنْ أَمْسَكَ رِزْقَهُۥۖ بَل لَّجُّواْ فِے عُتُوّٖ وَنُفُورٍۖ 21
أَفَمَنْ يَّمْشِے مُكِبّاً عَلَىٰ وَجْهِهِۦٓ أَهْدَىٰٓ أَمَّنْ يَّمْشِے سَوِيّاً عَلَىٰ صِرَٰطٖ
مُّسْتَقِيمٖۖ 22 قُلْ هُوَ اَلذِے أَنشَأَكُمْ وَجَعَلَ لَكُمُ السَّمْعَ وَالْأَبْصَٰرَ
وَالْأَفْـِٔدَةَۖ قَلِيلاٗ مَّا تَشْكُرُونَۖ 23 قُلْ هُوَ اَلذِے ذَرَأَكُمْ فِے الْأَرْضِ
وَإِلَيْهِ تُحْشَرُونَۖ 24 وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا اَلْوَعْدُ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَۖ 25
قُلْ إِنَّمَا اَلْعِلْمُ عِندَ اَللَّهِ وَإِنَّمَا أَنَا نَذِيرٞ مُّبِينٞۖ 26

ثمن

13. Hak̃ik̃a wad̃anda suke tsoron Ubangijinsu a halin rabuwarsu da idon mutane (suke binsa a ɓoye, da sarari kuma zai kasance minbabi'aula) gafara zata kasance garesu da lada mai girma.

(WANI ABU DAGA MABAYYANAR ƘUDURAR ALLAH DA NI'IMARSA DA ILIMINSA)

14. Ku ɓoye maganarku (yaku mutane) koku bayyana dashi, Ubangiji masanine da halin zukatan bayi, (bare abinda aka furta dashi, Sababin saukar wannan cewa mushirkai ba'alinsu ya gayawa ba'ali, "ku ɓoye maganarku kada Ubangijin Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama yajiku.)
15. Shin wanda ya halicci (wanda kuke asiri dashi) bazai san wannan asiri ba? Alhali Shine mai taushi a cikin saninsa mai isa matuk̃a a cikin sani? (Zai sani.)
16. Shine wanda yasanya k̃asa abar horewa gareku, kuyi tafiya a cikin sassan k̃asa, Kuci daga arzikinsa, (wanda ya halitta donku,) izuwa gareshi za a taraku (don sakamako.)
17. Shin kwa amince wanda ikonsa yake sama ya kisfe k̃asa daku, sai gata tana dandangurza daku.
18. Ko kwa amince wanda yake sama ya sako muku iska mai tsakwankwani? Da sannu zaku sani (yayin ganin azaba) yaya gargadina da azaba ya kasance? (Zaku san gaskiya ne.)
19. Hak̃ik̃a wad̃anda suke gabansu na daga al'ummatai sun k̃aryata manzanni yaya inkarina (yayin halakar dasu? gaskiya ne.) Ya afku gurin afkuwarsa).
20 Shin basuyi duba izuwa tsuntsaye ba burbushinsu a cikin sararin sama, suna masu shimfid̃e fikafikansu, suna masu tareta, ba abinda ya rik̃esu ga buran fad̃owa sai Allah Arrahamanu da k̃udurarsa, hak̃ik̃a shi masanine da komai, (watau bazasu kafa dalili da tsuntsaye a cikin sararin sama ba, a kan ikonmu, mu aikata abinda ya gabata dasu, hakanan waninsa na azaba? (Ma aikata).
21. Shin wane abune wanda yake runduna ne gareku, da yake taimakonku ba Allah ba? (Babu,) su kafirai basu kasance basai cikin rud̃i, (shaid̃an ya rud̃esu da cewa azaba bazata riskesu ba.)
22. Shin wanene wanda yake azurtaku, in Arrahamanu ya kame arzikinsa? (wato ruwa, ba mai azurta muku sai shi,) bari! Sun zarce cikin girmankai da gudu ga buran gaskiya.
23. Shin to wanda yake tafe yana kife a kan fuskarsa, shi yafi shiriya, ko wanda yake tafe daram a kan tafarki ma daidaici, (wannan misalin muminine da kafiri, wannenen sune a kan shiriya?)
24. Cene "Ubangiji ne ya halittar muku da kunnuwa da idonduna da zukata, kad̃anne k̃warai kuke godewa Allah.)
25. Cene "Shine wanda ya halicceku a cikin k̃asa izuwa gareshi ake taraku."

(TABBATAR DA TASHIN ALƘIYAMA DA BAYANIN BA'ALIN NI'IMOMI)

26. Suna fad̃a ga muminai yaushe ne wannan tashin alk̃iyamar inkun kasance magasgata (cikinsa?).

فَلَمَّا رَأَوْهُ زُلْفَةً سِيٓئَتْ وُجُوهُ الذِينَ كَفَرُواْ وَقِيلَ هَٰذَا الذِے
كُنتُم بِهِۦ تَدَّعُونَ ﴿27﴾ قُلْ أَرَآيْتُمْ إِنْ أَهْلَكَنِيَ اللَّهُ وَمَن مَّعِيَ أَوْ رَحِمَنَا
فَمَنْ يُّجِيرُ الْكٰفِرِينَ مِنْ عَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿28﴾ قُلْ هُوَ الرَّحْمٰنُ ءَامَنَّا بِهِۦ
وَعَلَيْهِ تَوَكَّلْنَا فَسَتَعْلَمُونَ مَنْ هُوَ فِے ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿29﴾ قُلْ أَرَآيْتُمْ
إِنْ أَصْبَحَ مَآؤُكُمْ غَوْراً فَمَنْ يَّأْتِيكُم بِمَآءٍ مَّعِينٍ ﴿30﴾

68 سُورَةُ الْقَلَمِ مَكِّيَّةٌ
وَهِيَ ثِنْتَانِ وَخَمْسُونَ ءَايَةً 52

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيمِ

نٓ وَالْقَلَمِ وَمَا يَسْطُرُونَ ﴿1﴾ مَا أَنتَ بِنِعْمَةِ رَبِّكَ بِمَجْنُونٍ ﴿2﴾ وَإِنَّ لَكَ
لَأَجْراً غَيْرَ مَمْنُونٍ ﴿3﴾ وَإِنَّكَ لَعَلَىٰ خُلُقٍ عَظِيمٍ ﴿4﴾ فَسَتُبْصِرُ
وَيُبْصِرُونَ ﴿5﴾ بِأَيِّيكُمُ الْمَفْتُونُ ﴿6﴾ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعْلَمُ بِمَن ضَلَّ
عَن سَبِيلِهِۦ وَهُوَ أَعْلَمُ بِالْمُهْتَدِينَ ﴿7﴾ فَلَا تُطِعِ الْمُكَذِّبِينَ ﴿8﴾
وَدُّواْ لَوْ تُدْهِنُ فَيُدْهِنُونَ ﴿9﴾ وَلَا تُطِعْ كُلَّ حَلَّافٍ مَّهِينٍ ﴿10﴾ هَمَّازٍ مَّشَّآءٍ
بِنَمِيمٍ ﴿11﴾ مَّنَّاعٍ لِّلْخَيْرِ مُعْتَدٍ أَثِيمٍ ﴿12﴾ عُتُلٍّ بَعْدَ ذَٰلِكَ زَنِيمٍ ﴿13﴾
أَن كَانَ ذَا مَالٍ وَبَنِينَ ﴿14﴾ إِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِ ءَايَٰتُنَا قَالَ أَسَٰطِيرُ الْأَوَّلِينَ ﴿15﴾

27. Cene "Dahir dai sanin zuwan tashin alƙiyama yana gurin Allah, ni mai gargaɗi ne mabayyanin gargaɗi kawai.
28. To zamanin da suka ga azabar nan a kusa, sai fuskokin waɗanda suka kafirta tayi baƙi ƙirin masu tsaron wuta sukace dasu, "Wannan azabar Shine abinda kuke da'awar babu shi".
29. Cene "ku bamu labarin in Ubangiji ya halakar dani da wanda yake taredani (na muminai da azabarsa tamfar da kuke nufi) ko yaji ƙanmu (bai mana azaba ba,) to waye zai tserar da kafirai daga azaba mai raɗaɗi?" (Babu.)
30. Cene "Shine Arrahamanu (wanda nake kiranku izuwa bauta masa,) mun bada gaskiya dashi, a gareshi kaɗai muka dogara, to da sannu zaku sani wanene yake cikin ɓata mabayyani (mu koku ko su.") yayin ganin azaba.
31. Cene "In ruwanku ya wayi gari a ƙafe wake zuwa muku da ruwa mai gudana, (da gonaki suke samunsa, ALLAHU RAB-BUL ALAMINA) To yaya kuke musuncewa zai tashe ku, (an soga mai karatun Alƙur'ani ƙarshen MA'IN yace ALLAHU RABBUL ALAMINA, tamfar da yazo a Hadisi an karanta wannan aya nan ga ba'alin Jabberai sai yace "diga da dundurusu," sai ruwan idonsa ya ƙafe a take a nan gurin ya makance. Muna neman tsari daga Allah a kan ƙarfin rai a kan ayoyinsa.)

Wannan Sura Itace Suratul Nuun

a Makka aka saukar da ita aya hamshin da biyuce (52)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe

(MUHAMMADU RASULULLAHI AKRAMU KHALKILLAHI)

(Ita wannan sura ta ƙunshi sifofin Annabi Sallallahu alaihi wasallama da shiryarwarsa da saɓawa insau ƙaryatawa da ƙissar ma'abota gona don firgitawa ga kafirai sannan munaƙasha dasu da ɓata hujjojinsu da umarnin Annabi Sallallahu alaihi wasallama da haƙuri kan cutarsu tareda bayanin tsananin ƙinsu da Annabi tareda Alƙur'ani).

1. Allahu a'alamu bi muradihi bi zalika, Allah ya rantse da alƙalami wanda ya rubuta kasantatu dashi a cikin Lauhil Mahfuzu, da abinda Mala'iku suke rubutawa (na alheri da gyara.)
2. Ya Annabi Muhammadu SallAllahu alaihi wasallama) ba mara hankaline kai ba, saboda ni'imar da Ubangiji yayi maka (da Annabci, wannan raddi ne bisa maganarsu cewa shi mara hankali ne.)
3. Haƙiƙa kana da lada ba abin yankewa ba, (mƙaminsa Sallallahu alaihi wasallama a cikin hauhauwa yake har abada kuma bayan mutuwarsa,yafi girma daga halin rayuwarsa, muƙaminsa a lahira yafi muƙaminsa a duniya kamar yadda Sawi ya faɗa.)
4. Ba shakka, haƙiƙa (ya shugabanmu) kana kan addini mai girma (wato Shine tadodin Alƙur'ani tadodinsa, kamar yadda Nana Aisha ta faɗa Allah ya ƙara yarda gareta
5. To da sannu zaka gani.kuma zasu gani
6. Wannenen kune fitina ta afku a gareshi, (a gareka ya Saiyidi ko a garesu.)
7. Haƙiƙa Ubangijinka Shine masani da wanda ya ɓace ga bulan hanyarsa, Shine masani da masu shiriya.
8. Kadaka daka ta masu ƙaryatawa.
9. Suna burin kai almundahana garesu (wato ka saida lahira ka karɓi duniya) to suma suyi haka a gareka.
10. Kada kabi dukkan mai yawan rantsuwa kan ƙarya, wulaƙantacce.
11. Mai yawan giba, mai yawan kaikawo da annamimanci (wato gulma).
12. Mai yawan hanawa ga alheri, (Shine rowa da dukiya ga wanda ya cancanta) azzalumi, fajiri, marar imani.
13. Bayan wannan kuma shege, (Shine Walidu ɗan Mugira, ubansa yayi ɗa'awarsa bayan shekara goma sha takwas, ibn Abbas yace "bamu sani cewa Allah Subhanahu wata'ala ya kamanta ɗaya da abinda ya kamantashi dashi na laifuka ba, ya riskar masa da abin faɗa wanda bazai rabu dashi ba har abada.")
14. Donya kasance ma'abocin dukiya da 'ya'yaye.
15. Idan ana karantawar ayoyinmu (na Alƙur'ani) a gareshi, sai yace ƙaryace-ƙaryacen mutanen farko ne."

ربع

سَنَسِمُهُۥ عَلَى ٱلۡخُرۡطُومِ (16) إِنَّا بَلَوۡنَٰهُمۡ كَمَا بَلَوۡنَآ أَصۡحَٰبَ ٱلۡجَنَّةِ إِذۡ أَقۡسَمُواْ
لَيَصۡرِمُنَّهَا مُصۡبِحِينَ (17) وَلَا يَسۡتَثۡنُونَ (18) * فَطَافَ عَلَيۡهَا طَآئِفٞ مِّن رَّبِّكَ
وَهُمۡ نَآئِمُونَ (19) فَأَصۡبَحَتۡ كَٱلصَّرِيمِ (20) فَتَنَادَوۡاْ مُصۡبِحِينَ (21) أَنِ ٱغۡدُواْ
عَلَىٰ حَرۡثِكُمۡ إِن كُنتُمۡ صَٰرِمِينَ (22) فَٱنطَلَقُواْ وَهُمۡ يَتَخَٰفَتُونَ (23)
أَن لَّا يَدۡخُلَنَّهَا ٱلۡيَوۡمَ عَلَيۡكُم مِّسۡكِينٞ (24) وَغَدَوۡاْ عَلَىٰ حَرۡدٖ قَٰدِرِينَ (25) فَلَمَّا
رَأَوۡهَا قَالُوٓاْ إِنَّا لَضَآلُّونَ (26) بَلۡ نَحۡنُ مَحۡرُومُونَ (27) قَالَ أَوۡسَطُهُمۡ أَلَمۡ أَقُل لَّكُمۡ
لَوۡلَا تُسَبِّحُونَ (28) قَالُواْ سُبۡحَٰنَ رَبِّنَآ إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ (29) فَأَقۡبَلَ بَعۡضُهُمۡ
عَلَىٰ بَعۡضٖ يَتَلَٰوَمُونَ (30) قَالُواْ يَٰوَيۡلَنَآ إِنَّا كُنَّا طَٰغِينَ (31) عَسَىٰ رَبُّنَآ
أَن يُبۡدِلَنَا خَيۡرٗا مِّنۡهَآ إِنَّآ إِلَىٰ رَبِّنَا رَٰغِبُونَ (32) كَذَٰلِكَ ٱلۡعَذَابُ
وَلَعَذَابُ ٱلۡأٓخِرَةِ أَكۡبَرُ لَوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ (33) إِنَّ لِلۡمُتَّقِينَ عِندَ رَبِّهِمۡ
جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ (34) أَفَنَجۡعَلُ ٱلۡمُسۡلِمِينَ كَٱلۡمُجۡرِمِينَ (35) مَا لَكُمۡ كَيۡفَ تَحۡكُمُونَ (36)
أَمۡ لَكُمۡ كِتَٰبٞ فِيهِ تَدۡرُسُونَ (37) إِنَّ لَكُمۡ فِيهِ لَمَا تَخَيَّرُونَ (38) أَمۡ لَكُمۡ أَيۡمَٰنٌ
عَلَيۡنَا بَٰلِغَةٌ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ إِنَّ لَكُمۡ لَمَا تَحۡكُمُونَ (39) سَلۡهُمۡ أَيُّهُم
بِذَٰلِكَ زَعِيمٌ (40) أَمۡ لَهُمۡ شُرَكَآءُ فَلۡيَأۡتُواْ بِشُرَكَآئِهِمۡ إِن كَانُواْ صَٰدِقِينَ (41)
يَوۡمَ يُكۡشَفُ عَن سَاقٖ وَيُدۡعَوۡنَ إِلَى ٱلسُّجُودِ فَلَا يَسۡتَطِيعُونَ (42)

16. Da sannu zamuyi masa alama a kan hancinsa, (aka tsage hancin da kansakali ranar Badar.)

(ƘISSAR MA'ABOTA GONA DA MANUFARTA)

17. Haƙiƙa mu mun jarrabi mutanen Makka (da fari da yunwa,) tamfar da muka jarrabi ma'abota gona, (gonace a Yemen anace dashi Sarwanu, koma bayan sana'a da farsahi biyu, mai gonar ya kasance yana tara fuƙara'u lokacin yanka, yabar musu abinda lauje yakuskure na hatsi, zamanin da suka rantse zasu yanketa da duru-duru, don kada faƙiran nan suji duriyarsu su hanasu abinda ubansu yake sadakar masu daga gonar.)
18. Basuyi togo ba (a cikin rantsuwarsu).
19. Sai mai kewayo daga Ubangijinka ya kewaya kansu, (wato wuta ta ƙoneta sarai da daddare) alhali su suna bacci.
20. Saita zama kamar dare baƙiƙƙirin.
21. Suka dinga kira da-duru-duru.
22. Kuyi sammako a kan amfanin gonarku in kuma nufin yankan hatsin.
23. Suka tafi alhali suna ɓuya.
24. Kada wani mabuƙaci ya shiga gareku a yau.
25. Sukayi sammako suna masu iko a kan hana talakawan nan sadaka.
26. To yayin da suka ganta a ƙone, sai sukace " haƙiƙa mu mun ɓace mata" (yayin da suka shaidata.)
27. Sai sukace "Kai! mudai an haramta ta garemu saboda mun hana talakawa haƙƙinta daga garemu.

(SHARRIN CUTAR TALAKAWA DA ANFANIN ZIKIRI TAREDATUBA)

28. Mufificinsu sai yace, "shin bance daku ,donme baku anbaci Allah kuna masu tuba gareshi
29. Sai sukace "Tsarki ya tabbatarwa Ubangijinmu, haƙiƙa mu mun kasance azzalumai da hanawan talakawa haƙƙinsu".
30. Sai ba'alinsu ya gabata kan ba'ali, suna zargin juna.
31. Sukace "wohoho ya halakarmu! mu haƙiƙa mun kasance masu dagawa.
32. "Muna ƙaunar Ubangiji ya musanya mana mafifici daga gareta, mu masu kwaɗayi ne izuwa Ubangijinmu (domin ya karɓi tubarmu, ya mayar mana da fiyeda abinda muka rasa, an ruwaito cewa an ruɓanya musu fiyeda ita.)"
33. Azaba (ga wanda ya saɓi umarninmu, kafiran Makka da waninsu,) irin wannan azabar mutane take. Kuma azabar lahira lallai tafi girma, dasun kasance sunsan (azaba tata, da basu saɓawa umarninmu ba.)

(MUNMASHAR MASU ƘARYATAWA DA FIRGITASU)

34. Haƙiƙa aljannatai na ni'ima sun tabbata ga masu tsoron Allah nan ga Ubangijinsu, (wannan aya ta sauka ne zamanin da sukace in an tashemu za a bamu fiyeda abinda kuke dashi.)
35. Shin toma sanya Musulmai kamar masu laifi? (Masu bi garesu cikin kyauta?)
36. Meke gareku? Yaya kuke hukunci (irin wannan hukunci mummuna?)
37. Bari! shinkuna da littafi ne abin saukarwa kuke karantawa a cikinsa?
38. Haƙiƙa cewa abinda kuke zaɓi haƙiƙa ya tabbata gareku a cikinsa.
39. Koko kuna da alƙawurane a kanmu ingantacciya izuwa ranar alƙiyama cewa kuna da abinda kuke hukuntawa? Wato haƙiƙa abinda kuke hukuntawa ya tabbata gareku? (babu).
40. Tambayesu, wannenensu ya lamince da wannan (cewa za a basu a lahira fiyeda abinda muminai suke dashi?)
41. Ko sharikai sun tabbata garesu ne? Masu dacewa dasu cikin wannan magana da suka lamince musu dashi? To in hakane; tosu zoda sharikannasu (masu lamince musu da haka ɗin,) in sun kasance masu gaskiya (a cikinsa).
42. Ambaci ranar da ake yayewa ga makengyama, (wato ranar da lamari yake tsananta, kuma ake kiransu ga sujada (don jarrabawa ga imaninsu,) bazasu sami dama ba, (don bayayyakinsu sun zama sandararriya.)

خَاشِعَةً أَبْصَارُهُمْ تَرْهَقُهُمْ ذِلَّةٌ وَقَدْ كَانُوا يُدْعَوْنَ إِلَى السُّجُودِ وَهُمْ
سَالِمُونَ ﴿43﴾ فَذَرْنِي وَمَن يُكَذِّبُ بِهَٰذَا الْحَدِيثِ سَنَسْتَدْرِجُهُم مِّنْ حَيْثُ
لَا يَعْلَمُونَ ﴿44﴾ وَأُمْلِي لَهُمْ إِنَّ كَيْدِي مَتِينٌ ﴿45﴾ أَمْ تَسْأَلُهُمْ أَجْرًا فَهُم مِّن مَّغْرَمٍ
مُّثْقَلُونَ ﴿46﴾ أَمْ عِندَهُمُ الْغَيْبُ فَهُمْ يَكْتُبُونَ ﴿47﴾ فَاصْبِرْ لِحُكْمِ رَبِّكَ وَلَا تَكُن
كَصَاحِبِ الْحُوتِ إِذْ نَادَىٰ وَهُوَ مَكْظُومٌ ﴿48﴾ لَّوْلَا أَن تَدَارَكَهُ نِعْمَةٌ
مِّن رَّبِّهِ لَنُبِذَ بِالْعَرَاءِ وَهُوَ مَذْمُومٌ ﴿49﴾ فَاجْتَبَاهُ رَبُّهُ فَجَعَلَهُ مِنَ
الصَّالِحِينَ ﴿50﴾ وَإِن يَكَادُ الَّذِينَ كَفَرُوا لَيُزْلِقُونَكَ بِأَبْصَارِهِمْ لَمَّا سَمِعُوا
الذِّكْرَ وَيَقُولُونَ إِنَّهُ لَمَجْنُونٌ ﴿51﴾ وَمَا هُوَ إِلَّا ذِكْرٌ لِّلْعَالَمِينَ ﴿52﴾

69 سُورَةُ الحَاقَّةِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ ثِنْتَانِ وَخَمْسُونَ ءَايَةً 52

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

ثمن

* الْحَاقَّةُ ﴿1﴾ مَا الْحَاقَّةُ ﴿2﴾ وَمَا أَدْرَاكَ مَا الْحَاقَّةُ ﴿3﴾ كَذَّبَتْ ثَمُودُ وَعَادٌ
بِالْقَارِعَةِ ﴿4﴾ فَأَمَّا ثَمُودُ فَأُهْلِكُوا بِالطَّاغِيَةِ ﴿5﴾ وَأَمَّا عَادٌ فَأُهْلِكُوا
بِرِيحٍ صَرْصَرٍ عَاتِيَةٍ ﴿6﴾ سَخَّرَهَا عَلَيْهِمْ سَبْعَ لَيَالٍ وَثَمَانِيَةَ أَيَّامٍ حُسُومًا
فَتَرَى الْقَوْمَ فِيهَا صَرْعَىٰ كَأَنَّهُمْ أَعْجَازُ نَخْلٍ خَاوِيَةٍ ﴿7﴾ فَهَلْ تَرَىٰ لَهُم مِّن بَاقِيَةٍ ﴿8﴾

43. Gannansu tana wulaƙance, (bazasu iya ɗagata sama ba) saboda wulaƙanci yana lulluɓesu, ana kiransu a duniya izuwa sujada, suna tafiya sumul, basu dungura goshiba.
44. To barni da wanda yake ƙaryata wannan zance (Alƙur'ani) da sannu zamuyi musu maƙarƙashiya mu riƙesu kaɗan kaɗan ta inda basu sani ba.
45. In yi jinkiri garesu, haƙiƙa shirina ƙaƙƙarfa ne (ba a immasa).
46. Bari! shin ka tambayesu lada bisa ida aikene? To su ababan nauyayawane (na daga abinda zasu baka shi.)
47. Shin akwai gaibune a gurinsu dasu suke rubutawan (abindasu suke faɗa daga shi.)

(ƘARSHEN ƘOSAWA DA GAGGAWA)

48. To daure da hukuncin Ubangijinka cikinsu da abinda yaga dama. Kadaka zamo tamfar ma'abocin kifi (a cikin ƙosawa da garaje Shine Annabi Yunusa Alaihissalamau) zamanin daya kira Ubangijinsa, alhali yana cike da baƙin ciki (a cikin kifi).
49. Badon rahamar Ubangijinsa ta riskeshi ba da an jefo shi daga cikin kifi a fako alhali yana abin zargi, (saidai shi Ubangiji yaji ƙansa aka jefar dashi ba abin zargi ba.)
50. Ubangijinsa yaza ɓeshi (da Annabci) Ya sanyashi cikin Annabawa salihai, (malam yana godiya ga Ubangiji daya azurta masa ziyara tasa dashiga gidansa, wanda haryau yana nan a gine da dutse, zamanai masu tsawo, kuma kabarinsa akwai nutsuwa daga Allah da mutum zai same ta a zuciya tasa, zamanin da yake muwajaha dashi.)

(TSANANIN ƘIYAYYA TA KAFIRAI GA MA'AIKIN ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAMA DA KIYON ALLAH GARESHI)

51. Haƙiƙa su kafirai sun kusa su zamo dakai da idandunansu, zamanin da sukaji Alƙur'ani (don hassada) suna cewa lallai shi bashi da hankali, (saboda Alƙur'anin dayazo dashi, wannan maganar Ubangiji yayi raddinta tun a farkon sura).
52. Shi Alƙur'ani bai kasance basai gargaɗi ga talikai (hauka baya faruwa gami dashi.)

Wannan Sura Itace Suratul Haƙƙatu

A Makka aka saukar da ita aya hamsin da biyuce (52)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan sura ta ƙunshi zance kan ranar alƙiyama da wanda ya ƙaryatada ita na daga al'umma da ƙarshensu da sifofin wannan rana da abinda mumini da kafiri zai gamu dashi da tabbatar da cewa Alƙur'ani Min-Indillahi ne da cewa haƙuri da dauriya da tasbihi Shine ya wajaba ga ma'aikin Allah (Sallallahu alaihi waSallama).

1. Tabbatacciya! Menene tabbatacciya? (Itace alƙiyama wacce take tabbatar da duk abinda aka musanta na tashi daga kabari da hisabi da sakamako. Kuma wannan tambaya girmamawane ga sha'aninta.)
2. Menene yasanar dakai Menene tabbatacciyar nan? (Ance ƙarin girmane ga sha'aninta.)
3. Samudu da Adu sun ƙaryata da mai ƙwanƙwasawa, (alƙiyama saboda tana tsorata zukata da tsarmakatanta.)
4. To amma Samudu, to an halakar dasu da matsananciyar tsawa (ta Mala'ika Jibrilu).
5. Adawa to an halakar dasu da iska mai tsananin amo da ƙarfi, a kan Adu tareda ƙarfinsu.
6. Ya sakota garesu, dare bakwai da wuni takwas, daga asubahin ranar Laraba 'takwas da suka ragu na Shawwal a ƙarshen dari, a jere. Kana ganin mutane a cikinta a kaye kai kace asalan dabinai ne, faɗaɗɗiya suna halake.
7. Shin kana ganin wani mai wanzuwa nasu?

وَجَآءَ فِرْعَوْنُ وَمَن قَبْلَهُۥ وَالْمُؤْتَفِكَٰتُ بِالْخَاطِئَةِ (8) فَعَصَوْا
رَسُولَ رَبِّهِمْ فَأَخَذَهُمْ أَخْذَةً رَّابِيَةً (9) إِنَّا لَمَّا طَغَا الْمَآءُ حَمَلْنَٰكُمْ
فِي الْجَارِيَةِ (10) لِنَجْعَلَهَا لَكُمْ تَذْكِرَةً وَتَعِيَهَآ أُذُنٌ وَاعِيَةٌ (11)
فَإِذَا نُفِخَ فِي الصُّورِ نَفْخَةٌ وَاحِدَةٌ (12) وَحُمِلَتِ الْأَرْضُ وَالْجِبَالُ
فَدُكَّتَا دَكَّةً وَاحِدَةً (13) فَيَوْمَئِذٍ وَقَعَتِ الْوَاقِعَةُ (14) وَانشَقَّتِ
السَّمَآءُ فَهِيَ يَوْمَئِذٍ وَاهِيَةٌ (15) وَالْمَلَكُ عَلَىٰٓ أَرْجَآئِهَا وَيَحْمِلُ
عَرْشَ رَبِّكَ فَوْقَهُمْ يَوْمَئِذٍ ثَمَٰنِيَةٌ (16) يَوْمَئِذٍ تُعْرَضُونَ لَا تَخْفَىٰ مِنكُمْ
خَافِيَةٌ (17) فَأَمَّا مَنْ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ فَيَقُولُ هَآؤُمُ اقْرَءُوا كِتَٰبِيَهْ (18)
إِنِّي ظَنَنتُ أَنِّي مُلَٰقٍ حِسَابِيَهْ (19) فَهُوَ فِي عِيشَةٍ رَّاضِيَةٍ (20) فِي جَنَّةٍ
عَالِيَةٍ (21) قُطُوفُهَا دَانِيَةٌ (22) كُلُوا وَاشْرَبُوا هَنِيٓـًٔا بِمَآ أَسْلَفْتُمْ فِي الْأَيَّامِ
الْخَالِيَةِ (23) وَأَمَّا مَنْ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِشِمَالِهِۦ (24) فَيَقُولُ يَٰلَيْتَنِي لَمْ أُوتَ كِتَٰبِيَهْ (25)
وَلَمْ أَدْرِ مَا حِسَابِيَهْ (26) يَٰلَيْتَهَا كَانَتِ الْقَاضِيَةَ (27) مَآ أَغْنَىٰ عَنِّي
مَالِيَهْ (28) هَلَكَ عَنِّي سُلْطَٰنِيَهْ (29) خُذُوهُ فَغُلُّوهُ (30) ثُمَّ الْجَحِيمَ صَلُّوهُ (31)
ثُمَّ فِي سِلْسِلَةٍ ذَرْعُهَا سَبْعُونَ ذِرَاعًا فَاسْلُكُوهُ (32) إِنَّهُۥ كَانَ
لَا يُؤْمِنُ بِاللَّهِ الْعَظِيمِ (33) وَلَا يَحُضُّ عَلَىٰ طَعَامِ الْمِسْكِينِ (34)

8. Fir'aunu da wađanda suke gabansa da mutanen Annabi Luđu sun zoda aiyuka na kuskure.
9. Suka sabi jakadan Ubangijinsu (Annabi Hudu Alaihissalamu da waninsa,) saiya danƙesu danƙa mai faifayawar tsanani a kan waninta.
10. Haƙiƙa mu zamanin da ruwa yayi zara (a kan duwarwatsu da waninta,) mun đauke ku, (wato iyayenku alhali ku kuna cikin tsatsonsu) a cikin jirgi mai gudana (ta Annabi Nuhu, shi da wađanda suke ciki suka tsira, shauran suka nutse.)
11. Donmu sanya wannan aiki (wato tserar da muminai da halakar da kafirai) ta zama gargađi gareku, kunne mai haddacewa ya haddace ta.

(RANAR HISABI DA ABINDA YAKE CIKINSA NA DAGA MATSAYEN MUTANEN KIRKI DA FAJIRAI)

12. Idan akai busa busa guda đaya a cikin ƙaho, (saboda rabe hukunci tsakanin talikai Itace ta biyu.)
13. Aka đaga ƙasa da duwarwatsu aka dandaƙesu dandaƙewa guda đaya.
14. A wannan ranane alƙiyama ta tashi.
15. Sama ta kece ita a wannan rana rarrauna ce.
16. Mala'iku suna sassanta, Mala'iku takwas suna đauke da Al'arshin Ubangijinka, burbushin wađancanenka Mala'iku ababan ambato.
17. A wannan rana ake bijirar daku ,izuwa hisabi, wata mai ɓuya bazata ɓuya da daga gareku na daga asirin bayi.
18. Amma wanda aka bashi littafinsa a hannun dama, zai fađa (ga jama'arsa, saboda abinda yayi farin ciki dashi,) "ku ungo littafina ku karantashi."
19. " Haƙiƙa na tabbata lallai ni mai gamuwa da sakamakona ne."
20. To wannan mutum yana cikin rayuwa abar yarda da ita.
21. A cikin aljanna mađaukakiya.
22. 'Ya'yan itatuwanta makusanta ne (na tsaye dana zaune dana kwance suna
23. Kuci kusha ababan farantawa ciki saboda abinda kuka gabotar a duniya.
24. Amma wanda aka bashi takardarsa a hagun đinsa.
25. Zaice "Wohoho daya kace ni ba a bani littafina ba!
26. "Ban san meye lissafina ba!
27. "Inama mutuwa (ta duniya) ta kasance Itace mai yankewa ga rayuwata, (baza a tashe ni ba!)
28. "Dukiya ta bata anfana min komai ba!
29. "'Hujja ta ta ɓace min!."
30. Ku danƙeshi (ku mataskata jahannama!). Ku tara hannayensa cikin ƙuƙumi. (Zuwa wuyansu).
31. Sannan ku shigashshe shi cikin jahannama.
32. Sannan ku shigar dashi (bayan shiga wuta) a cikin sarƙa, kamunta zira'i saba'in (70) (da zira'in Mala'iku.) Ku shigar dashi a cikin ta bayan ya shiga wuta).
33. Haƙiƙa shiya kasance bai bada gaskiya da Allah mai girma ba.
34. Baya kwađaitar da kansa ko waninsa kan ciyar da miskini mabuƙaci.



فَلَيْسَ لَهُ ٱلْيَوْمَ هَٰهُنَا حَمِيمٌ ﴿35﴾ وَلَا طَعَامٌ إِلَّا مِنْ غِسْلِينٍ ﴿36﴾ لَّا يَأْكُلُهُۥٓ
إِلَّا ٱلْخَٰطِـُٔونَ ﴿37﴾ ۞ فَلَآ أُقْسِمُ بِمَا تُبْصِرُونَ ﴿38﴾ وَمَا لَا تُبْصِرُونَ ﴿39﴾
إِنَّهُۥ لَقَوْلُ رَسُولٍ كَرِيمٍ ﴿40﴾ وَمَا هُوَ بِقَوْلِ شَاعِرٍ قَلِيلًا مَّا تُؤْمِنُونَ ﴿41﴾
وَلَا بِقَوْلِ كَاهِنٍ قَلِيلًا مَّا تَذَكَّرُونَ ﴿42﴾ تَنزِيلٌ مِّن رَّبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿43﴾
وَلَوْ تَقَوَّلَ عَلَيْنَا بَعْضَ ٱلْأَقَاوِيلِ ﴿44﴾ لَأَخَذْنَا مِنْهُ بِٱلْيَمِينِ ﴿45﴾ ثُمَّ لَقَطَعْنَا
مِنْهُ ٱلْوَتِينَ ﴿46﴾ فَمَا مِنكُم مِّنْ أَحَدٍ عَنْهُ حَٰجِزِينَ ﴿47﴾ وَإِنَّهُۥ لَتَذْكِرَةٌ
لِّلْمُتَّقِينَ ﴿48﴾ وَإِنَّا لَنَعْلَمُ أَنَّ مِنكُم مُّكَذِّبِينَ ﴿49﴾ وَإِنَّهُۥ لَحَسْرَةٌ
عَلَى ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿50﴾ وَإِنَّهُۥ لَحَقُّ ٱلْيَقِينِ ﴿51﴾ فَسَبِّحْ بِٱسْمِ رَبِّكَ ٱلْعَظِيمِ ﴿52﴾

70 سُورَةُ المَعَارِجِ مَكِّيَّة
وَهِيَ أَرْبَعٌ وَأَرْبَعُونَ ءَايَة 44

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

سَأَلَ سَآئِلٌۢ بِعَذَابٍ وَاقِعٍ ﴿1﴾ لِّلْكَٰفِرِينَ لَيْسَ لَهُۥ دَافِعٌ ﴿2﴾ مِّنَ ٱللَّهِ ذِى ٱلْمَعَارِجِ ﴿3﴾
تَعْرُجُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَٱلرُّوحُ إِلَيْهِ فِى يَوْمٍ كَانَ مِقْدَارُهُۥ خَمْسِينَ أَلْفَ سَنَةٍ ﴿4﴾
فَٱصْبِرْ صَبْرًا جَمِيلًا ﴿5﴾ إِنَّهُمْ يَرَوْنَهُۥ بَعِيدًا ﴿6﴾ وَنَرَىٰهُ قَرِيبًا ﴿7﴾ يَوْمَ تَكُونُ ٱلسَّمَآءُ
كَٱلْمُهْلِ ﴿8﴾ وَتَكُونُ ٱلْجِبَالُ كَٱلْعِهْنِ ﴿9﴾ وَلَا يَسْـَٔلُ حَمِيمٌ حَمِيمًا ﴿10﴾

35. To a yau bashi da wani aboki dazai anfani dashi.
36. Wala abnci sai surƙamin 'yan wuta.
37. Ban da kafirai ba mai cinsa.

(HAƘIƘAR ALƘUR'ANI DA ABINDA AKA SAUKAR CIKINSA)

38. Ina rantsuwa da abinda kuke gani (na daga abin halitta).
39. Da abinda bakwa gani (na talikai.)
40. Haƙiƙa Alƙur'ani lallai maganar manzo ne mai girma (ya faɗeshi don aike daga Allah ta'ala,)
41. Shiba maganar mawaƙine ba, kaɗan ne ƙwarai kuke bada gaskiya.
42. Ba maganar bokane ba. kaɗanne ƙwarai kuke wa'azantuwa.
43. Shidai saukakkene daga Ubangijin talikai.
44. Da Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) zai ƙirƙiri ba'alin ma ganganu a garemu. ya faɗi abinda bamu gaya masa ba.
45. Da munyi riƙo daga gareshi da dama (wato da mun masa riƙon tsauri.)
46. Sannan da mun yanke masa jijiyar zuciya (wanda inya tsinke mutum yake mutuwa.)
47. To babu wani mutum daga gareku masu tarewa ga buransa.
48. Haƙiƙa shi Alƙur'ani gargaɗine ga masu jin tsoron Allah.
49. Haƙiƙa mun sani daga cikinku ku mutane akwai masu ƙaryatawa da Alƙur'ani (kuma akwai masu gasgatawa dashi.)
50. Haƙiƙa Alƙur'ani nadamane ga kafirai (idan sun ga ladan masu gasgatawa da uƙubar masu ƙaryatawa.)
51. Haƙiƙashi Alƙur'ani sakankancewa ce ta gaskiya.
52. To tsarkake sunan Ubangijinka mai girma.

Wannan Sura Itace Suratul Ma'uriji

A Makka aka saukar da ita aya arba'in da huɗu ce (44)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan sura ta ƙunshi firgita mushurkai da sifar ranar alƙiyama da magana kan sifar mutum da ɗabi'arsa da maganinsa, sannan ban tsoron ga mushurkai).

1. Mai addu'a yayi addu'a ga azaba mai afkuwa.
2. Ga kafirai (Naliru ɗan Harisune yayi addu'ar yace "Ubangiji in wannan ya kasance Shine da gaskiya daga gareka, a saukai musu da dutse daga sama, to Wallahi bai sadu izuwa taguwarsa ba face an jefe shi da dutse a ƙwaƙwalwarsa, yafito ta duburarsa sai wannan aya ta sauka. Kuma shi azabar) babu mai tureshi.
3. Daga Ubangiji ma'abocin tsaneku (na hawan Mala'iku izuwa sama.)
4. Mala'iku suna hawa da Mala'ika Jibrilu izuwa gareshi, (izuwa masaukar al'amarin Ubangiji na sama) a cikin rana wanda miƙdarinsa shekara dubu hamsin (dangane ga kafiri saboda abinda yake faɗawa cikinsa na daga tsanance-tsanance amma mumini zai kasance mafi sauƙi daga salla ɗaya ta farilla da yake sallatarta a duniya) kamar dayazo cikin hadisi.
5. Toyi haƙuri haƙuri mai kyau, (gaban yin umarnina da yaƙi,)
6. Haƙiƙa su suna ganin wannan azaba (mai nisa ba mai afkuwa ba.)
7. Muna ganinsa makusanci (mai afkuwa dole ba kokwanto.
8. Ranar da sama take kasancewa kamar narkakkiyar azurfa.
9. Duwarwatsu suke zama kamar angalalan auduga (ko gashi a cikin sheƙewa a sama).
10. Aboki baya tambayar aboki (saboda ya shagala da halin da yake cikinsa).

يُبَصَّرُونَهُمْ يَوَدُّ الْمُجْرِمُ لَوْ يَفْتَدِے مِنْ عَذَابِ يَوْمَئِذِۢ بِبَنِيهِ ﴿11﴾
وَصَاحِبَتِهِۦ وَأَخِيهِ ﴿12﴾ وَفَصِيلَتِهِ الَّتِے تُـٔوِيهِ ﴿13﴾ وَمَن فِے الْأَرْضِ
جَمِيعاً ثُمَّ يُنجِيهِ ﴿14﴾ كَلَّا إِنَّهَا لَظ۪ىٰ ﴿15﴾ نَزَّاعَةٌ لِّلشَّو۪ىٰ ﴿16﴾ تَدْعُواْ مَنْ
أَدْبَرَ وَتَوَلّ۪ىٰ ﴿17﴾ وَجَمَعَ فَأَوْع۪ىٰ ﴿18﴾ * إِنَّ الْإِنسَانَ خُلِقَ هَلُوعاً ﴿19﴾ ثمن
إِذَا مَسَّهُ الشَّرُّ جَزُوعاً ﴿20﴾ وَإِذَا مَسَّهُ الْخَيْرُ مَنُوعاً ﴿21﴾ إِلَّا الْمُصَلِّينَ ﴿22﴾
الَّذِينَ هُمْ عَلَىٰ صَلَاتِهِمْ دَآئِمُونَ ﴿23﴾ وَالَّذِينَ فِے أَمْوَالِهِمْ حَقٌّ مَّعْلُومٌ ﴿24﴾
لِّلسَّآئِلِ وَالْمَحْرُومِ ﴿25﴾ وَالَّذِينَ يُصَدِّقُونَ بِيَوْمِ الدِّينِ ﴿26﴾
وَالَّذِينَ هُم مِّنْ عَذَابِ رَبِّهِم مُّشْفِقُونَ ﴿27﴾ إِنَّ عَذَابَ رَبِّهِمْ غَيْرُ مَأْمُونٍ ﴿28﴾
وَالَّذِينَ هُمْ لِفُرُوجِهِمْ حَٰفِظُونَ ﴿29﴾ إِلَّا عَلَىٰ أَزْوَاجِهِمْ أَوْ مَا مَلَكَتْ أَيْمَانُهُمْ
فَإِنَّهُمْ غَيْرُ مَلُومِينَ ﴿30﴾ فَمَنِ ابْتَغ۪ىٰ وَرَآءَ ذَٰلِكَ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ
الْعَادُونَ ﴿31﴾ وَالَّذِينَ هُمْ لِأَمَٰنَٰتِهِمْ وَعَهْدِهِمْ رَاعُونَ ﴿32﴾ وَالَّذِينَ
هُم بِشَهَادَتِهِمْ قَآئِمُونَ ﴿33﴾ وَالَّذِينَ هُمْ عَلَىٰ صَلَاتِهِمْ يُحَافِظُونَ ﴿34﴾
أُوْلَٰٓئِكَ فِے جَنَّٰتٍ مُّكْرَمُونَ ﴿35﴾ فَمَالِ الَّذِينَ كَفَرُواْ قِبَلَكَ مُهْطِعِينَ ﴿36﴾
عَنِ الْيَمِينِ وَعَنِ الشِّمَالِ عِزِينَ ﴿37﴾ أَيَطْمَعُ كُلُّ امْرِےٕ مِّنْهُمْ
أَن يُدْخَلَ جَنَّةَ نَعِيمٍ ﴿38﴾ كَلَّا إِنَّا خَلَقْنَٰهُم مِّمَّا يَعْلَمُونَ ﴿39﴾

11. Ana nunawa abokai abokakansu, (su san juna amma bazasu iya zance ba,) kafiri yana burin dama yayi fansa daga azabar wannan rana da 'ya'yansa.
12. Da matarsa da 'yan uwansa.
13. Da ƙabilarsa wacce take rungume shi.
14. Da wanda yake cikin ƙasa baki ɗaya sannan wannan fansa ya tserar dashi.
15. Ina! Ita wuta Lazzace saboda tana horuwa ga kafirai.
16. Mai toyewa ga fatar kai.
17. Tana kiran wanda ya bada bayaya girka a guje (ga buran imani tana cewa "gareni gareni.")
18. Ya tara dukiya ya tamke (bai fitar da haƙƙin Allah daga gareshi ba.)

(ƊABI'AR MUTUM DA MAGANIN ALƘUR'ANI GARETA)

19. Haƙiƙa mutum an halicce shimai ƙawar zuci.
20. Mai firgita. idan sharri ya sameshi (watau idan sharri ya sameshi mai raki).
21. Idan alheri ya sameshi mai hanawa.

(SALLAR MASANA UBANGIJI)

22. Sai Muminai,
23. Waɗandasu suke dauwama ne a kan salla tasu.
24. Waɗanda suke akwai haƙƙi abin sani a dukiyoyinsu, (Shine zakka.)
25. Ga wanda yake mai tambaya da wanda yake abin haramtawa (shine wanda ya kame kansa ga buran roƙon ba a bashi ba).
26. Da waɗanda suke gasgatawa da ranar sakamako.
27. Da waɗanda suke masu tsoro ga azabar Ubangijinsu.
28. Haƙiƙa azabar Ubangijinsu ba abin amincewar saukarsa ne ba.
29. Da waɗanda suke masu kiyayewa ga farjojinsu.
30. Sai bisa matayensu. ko abinda hannunsu ya mallaka (na daga kuyangi,) haƙiƙa su ba ababan zargi bane (a kan haka.)
31. To duk wanda ya nemi wanin wancanenka, to wancanenka sune ainihin masu shishshigi.
32. Da waɗanda suke sune masu kiyayewa da amanoninsu da alƙawarinsu.
33. Da waɗanda sukesu masu tsayawa ne da shaidarsu (zasu bada ita bazasu ɓoyeta ba.)
34. Da waɗanda sukesu masu kiyayewa ne ga salla tasu (masu bada itane cikin farkon lokatanta.)
35. Waɗancananka suna cikin aljannatai ababan girmamawa ne.
36. To Menene ga waɗanda suka kafirta daura da kai, suke masu dauwamar da duba.
37. Daban daban daura da kai. waɗansu ga buran damanka waɗansu ga buran hauninka, (don izgili suna faɗa don izgili ga muminai, Wallahi in waɗannan sun shiga aljanna zamu shige ta gabansu.)
38. Yanzu kowane mutum daga garesu yayi zaton a shigar dashi aljanna ta ni'ima?
39. Haggyala! Haƙiƙa mu mun halicce su (kamar waninsu) daga abinda suka sani daga majinar mani, ta baza ayi tsammanin shiga aljannah da wannan ba, za ayi tsammanin shiga aljanna da taƙawa ne kawai.)



* فَلَا أُقْسِمُ بِرَبِّ الْمَشَٰرِقِ وَالْمَغَٰرِبِ إِنَّا لَقَٰدِرُونَ ﴿40﴾ عَلَىٰٓ أَن نُّبَدِّلَ
خَيْراً مِّنْهُمْ وَمَا نَحْنُ بِمَسْبُوقِينَ ﴿41﴾ فَذَرْهُمْ يَخُوضُواْ وَيَلْعَبُواْ حَتَّىٰ يُلَٰقُواْ
يَوْمَهُمُ الَّذِي يُوعَدُونَ ﴿42﴾ يَوْمَ يَخْرُجُونَ مِنَ الْأَجْدَاثِ سِرَاعاً كَأَنَّهُمْ إِلَىٰ نُصُبٍ
يُوفِضُونَ ﴿43﴾ خَٰشِعَةً أَبْصَٰرُهُمْ تَرْهَقُهُمْ ذِلَّةٌ ذَٰلِكَ الْيَوْمُ الَّذِي كَانُواْ يُوعَدُونَ ﴿44﴾

سُورَةُ نُوحٍ مَكِّيَّةٌ 71
وَهِيَ ثَلَاثُونَ ءَايَةً 30

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

إِنَّا أَرْسَلْنَا نُوحاً إِلَىٰ قَوْمِهِ أَنْ أَنذِرْ قَوْمَكَ مِن قَبْلِ أَن يَأْتِيَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿1﴾
قَالَ يَٰقَوْمِ إِنِّي لَكُمْ نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿2﴾ أَنُ اعْبُدُواْ اللَّهَ وَاتَّقُوهُ وَأَطِيعُونِ ﴿3﴾
يَغْفِرْ لَكُم مِّن ذُنُوبِكُمْ وَيُؤَخِّرْكُمْ إِلَىٰ أَجَلٍ مُّسَمًّى إِنَّ أَجَلَ اللَّهِ
إِذَا جَآءَ لَا يُؤَخَّرُ لَوْ كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿4﴾ قَالَ رَبِّ إِنِّي دَعَوْتُ قَوْمِي لَيْلاً
وَنَهَاراً ﴿5﴾ فَلَمْ يَزِدْهُمْ دُعَآءِي إِلَّا فِرَاراً ﴿6﴾ وَإِنِّي كُلَّمَا دَعَوْتُهُمْ
لِتَغْفِرَ لَهُمْ جَعَلُواْ أَصَٰبِعَهُمْ فِي ءَاذَانِهِمْ وَاسْتَغْشَوْاْ ثِيَابَهُمْ وَأَصَرُّواْ
وَاسْتَكْبَرُواْ اسْتِكْبَاراً ﴿7﴾ ثُمَّ إِنِّي دَعَوْتُهُمْ جِهَاراً ﴿8﴾ ثُمَّ إِنِّي أَعْلَنتُ لَهُمْ
وَأَسْرَرْتُ لَهُمْ إِسْرَاراً ﴿9﴾ فَقُلْتُ اسْتَغْفِرُواْ رَبَّكُمْ إِنَّهُ كَانَ غَفَّاراً ﴿10﴾

40. To lallai ina rantsuwa da Ubangijin mahudar rana da matadarta (da sauran taurari.) haƙiƙa mu masu ikone.
41. A kanmu zoda fiye daga garesu mu bamu kasance masu gazawa ba (da wancanenka.)
42. Ka barsu su kutsa a cikin wasanninsu suyi wasa (a duniyarsu,) harsu gamu da ranarsu wadda ake musu alƙawari cikinsa.
43. Ranar dasuke fitowa daga kaburburansu a guje (izuwa taron alƙiyama.)
44. Kai kece suna gudu izuwa abin kafawa (na tuta ko waninta.) halin kasancevvar idonsu wuƙakantacciya. Wuƙakanci yana lulluɓesu wancanenka Shine rana da suka kasance anayi musu alwashinsa, (ranar alƙiyama.)

Wannan Sura Itace Suratu Nuhu Alaihissalamu

A Makka aka saukar da ita aya talatin ce (30)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan sura ta ƙunshi ƙissar Annabi Nuhu Alaihissalamu da falalar istigfari da kirari ga Allah da addu'ar Annabi Nuhu Alaihissalamu ga dukkan muminai maza da mata).

(ƘISSAR ANNABI NUHU DA MUTANENSA)

1. Haƙiƙa mun aiko Annabi Nuhu izuwa mutanensa (wato mutanen dukkan ƙasa) cewa kayiwa mutanenka gargaɗi tun gaban azaba mai raɗaɗi baizo musu ba (a duniyain basu bada gaskiya ba.)
2. Yace "Yaku mutanena! haƙiƙa ni mai gargaɗi ne mabaiyanin gargaɗi a garcku (Shine ince daku).
3. "Ku bautawa Allah kuji tsoronsa, kubini."
4. "Ya gafarta muku zunubanku, zai jinkirta muku bada azaba ba izuwa ajali abin ambato (Shine mutuwa,) haƙiƙa ajalin Ubangiji (da azaba inbaku bada gaskiya ba,) in yazo ba a jinkirtashi ba, dakun kasance kunsan (haka da kun bada gaskiya.")
5. Yace "Ubangijina! haƙiƙani na kirawo mutanena dare da rana.
6. "Kirana bai ƙara musu kome ba, sai gudu (ga buran imani".)
7. " Haƙiƙa ni koyaushe na kirasu don kayi gafara garesu, saisu sanya kawunan 'yan yatsunsu a cikin kunnuwansu (don kada suji magana ta,) su lulluɓe kawukansu da tufafinsu (don kadasu ganni,) su zarce kan kafircinsu suyi girman kai (ga buran imani,) girman kai.
8. "Sannan haƙiƙa nina kirasu a sarari ƙarara.
9. "Sannan haƙiƙa nina baiyana musu muryata, na kuma ɓoye musu zance ɓoyewa.

(FALALAR ISTIGFARI)

10. Nace "Ku nemi gafarar Ubangijinku haƙiƙa shiya tabbata mai yawan gafara."

ثمن

يُرْسِلِ السَّمَاءَ عَلَيْكُم مِّدْرَارًا ﴿11﴾ وَيُمْدِدْكُم بِأَمْوَالٍ وَبَنِينَ
وَيَجْعَل لَّكُمْ جَنَّاتٍ وَيَجْعَل لَّكُمْ أَنْهَارًا ﴿12﴾ مَا لَكُمْ لَا تَرْجُونَ
لِلَّهِ وَقَارًا ﴿13﴾ وَقَدْ خَلَقَكُمْ أَطْوَارًا ﴿14﴾ * أَلَمْ تَرَوْا كَيْفَ خَلَقَ اللَّهُ
سَبْعَ سَمَاوَاتٍ طِبَاقًا ﴿15﴾ وَجَعَلَ الْقَمَرَ فِيهِنَّ نُورًا وَجَعَلَ الشَّمْسَ
سِرَاجًا ﴿16﴾ وَاللَّهُ أَنبَتَكُم مِّنَ الْأَرْضِ نَبَاتًا ﴿17﴾ ثُمَّ يُعِيدُكُمْ فِيهَا وَيُخْرِجُكُمْ
إِخْرَاجًا ﴿18﴾ وَاللَّهُ جَعَلَ لَكُمُ الْأَرْضَ بِسَاطًا ﴿19﴾ لِّتَسْلُكُوا مِنْهَا سُبُلًا
فِجَاجًا ﴿20﴾ قَالَ نُوحٌ رَّبِّ إِنَّهُمْ عَصَوْنِي وَاتَّبَعُوا مَن لَّمْ يَزِدْهُ مَالُهُ
وَوَلَدُهُ إِلَّا خَسَارًا ﴿21﴾ وَمَكَرُوا مَكْرًا كُبَّارًا ﴿22﴾ وَقَالُوا لَا تَذَرُنَّ
آلِهَتَكُمْ وَلَا تَذَرُنَّ وُدًّا وَلَا سُوَاعًا ﴿23﴾ وَلَا يَغُوثَ وَيَعُوقَ وَنَسْرًا
وَقَدْ أَضَلُّوا كَثِيرًا ﴿24﴾ وَلَا تَزِدِ الظَّالِمِينَ إِلَّا ضَلَالًا ﴿25﴾ مِّمَّا خَطِيئَاتِهِمْ
أُغْرِقُوا فَأُدْخِلُوا نَارًا ﴿26﴾ فَلَمْ يَجِدُوا لَهُم مِّن دُونِ اللَّهِ
أَنصَارًا ﴿27﴾ وَقَالَ نُوحٌ رَّبِّ لَا تَذَرْ عَلَى الْأَرْضِ مِنَ الْكَافِرِينَ
دَيَّارًا ﴿28﴾ إِنَّكَ إِن تَذَرْهُمْ يُضِلُّوا عِبَادَكَ وَلَا يَلِدُوا إِلَّا فَاجِرًا
كَفَّارًا ﴿29﴾ رَّبِّ اغْفِرْ لِي وَلِوَالِدَيَّ وَلِمَن دَخَلَ بَيْتِيَ مُؤْمِنًا
وَلِلْمُؤْمِنِينَ وَالْمُؤْمِنَاتِ وَلَا تَزِدِ الظَّالِمِينَ إِلَّا تَبَارًا ﴿30﴾

11. "Ya sako ruwa a gareku, mai yawan kwarara (alhali an hanasu ruwan.)
12. "Zai ƙareku da ɗukiyoyi da 'ya'yaye masu yawa zai sanya muku ƙoramu masu ƙwarara.
13. "Menene gareku bakwa ƙaunar girmamawar Allah gareku (wakarune mai ma'anar taukiru, Shine ku bada gaskiya).
14. "Haƙiƙa na halicceku hali bayan hali (Nuɗufa wani yayi alƙahhar izuwa cikar hallttar mutum tunani cikin halittar mutum yana ƙara imani ga mahalicci subhanahu wata'ala.)
15. "Shin bakwa lura, yaya Ubangiji ya halicci sammai bakwai ruɓi-ruɓi'?
16. "Ya sanya wata a cikinsu haske,ya sanya rana fitila mai ƙyalli.
17. "Ubangijine ya halicceku daga ƙasa (donya halicci babanku Annabi Adamu Alaihissalamu daga gareta) halitta.
18. "Sannan zai maidaku ,cikinta (kuna cikin kushewa,) zai fitar daku ,(saboda tashin alƙiyama fitarwa.
19. "Allah ya sanya muku ƙasa shimfiɗa".
20. Donku shiga hanyoyi daga gareta mayalwata.
21. Annabi Nuhu yace "Ya Ubangiji haƙiƙa su sun saɓeni, su ƙanƙanana sunbi wanda dukiyarsa da 'ya'yayensa basu ƙara masa komai baSai taɓewa" (gurin Ubangiji, sune shuwagabannin da aka ambacesu da wancanenka.)
22. SU shuwagabannin nan sun shirya makirci makirci mai girma. (Shine suka ƙaryata Annabi Nuhu suka cuceshi da wanda yabi shi.)
23. Sukace da ƙananan "kadaku ,bar bautar iyayen gijinku kada kubar Waddu kada kubar Suwa'u.
24. "Hakana Yagusu da yaƙuƙuda Nasru;'
25. " Haƙiƙa sun ɓatar da yawa-yawa na mutane. Kada ka ƙarawa azalumai sai ɓata (Alhali na ɓatar dasu ɗin, yayi musu mugunyar addu'a zamanin da aka sanar dashi iyakar waɗanda suka bada gaskiya dashi.)
26. Saboda kurakuransune aka halakar dasu (da ɗufanu,) aka shigar dasu wuta (wato akayi musu uƙuba da ita bayanan musu uƙuba da ruwa.)
27. Basu sami masu taimako ba, ba Allah ba, (dazai hana musu azaba ba,)
28. Annabi Nuhu yace "Ubangiji! Kada kabar zanzaro a kan ƙasa na daga kafirai (wato mutum ɗaya wanda zai zauna a gida).
29. " Haƙiƙa Ubangijiin ka barsu sa ɓatar da bayinka, bazasu haifa basai kafirai, (ya faɗi wannan saboda abinda yagabata na wahayi gareshi).

(KULAWAR ANNABI NUHU ALAIHISSALAMU A KAN KULAWA DA ZURIYARSA IZUWA TASHIN ALƘIYAMA. ALLAH YA SAKA MASA DA ALHERI)

30. "Ubangiji kai gafara gareni da mahaifana kai gafara ga wanda ya shiga ɗakina yana mumini (Baiti Ance gidana ko masallacina yafi kyau ya zama masallacinsa, Malam yana godewa Allah Ubangiji da yayi baiwa Malam ya shiga masallacin nasa, Shine Masallacin Kuta wanda a cikinsa ne aka kashe Sayyidina Ali Allah ya ƙara masa yarda.) Kai gafara ga muminai mazaje da mataye izuwa ranar alƙiyama, kadaka ƙarawa kafirai sai halaka," (aka halakar dasu).

72 سُورَةُ الجِنِّ مَكِّيَّة
وَهِيَ ثَمَانٍ وَعِشْرُونَ ءَايَة 28

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

حزب

* قُلُ اُوحِيَ إِلَيَّ أَنَّهُ اُسْتَمَعَ نَفَرٌ مِّنَ اَلْجِنِّ فَقَالُوا إِنَّا سَمِعْنَا قُرْءَانًا
عَجَبًا ﴿1﴾ يَهْدِي إِلَى اَلرُّشْدِ فَـَٔامَنَّا بِهِۦ وَلَن نُّشْرِكَ بِرَبِّنَا أَحَدًا ﴿2﴾ وَإِنَّهُۥ تَعَٰلَىٰ
جَدُّ رَبِّنَا مَا اَتَّخَذَ صَٰحِبَةً وَلَا وَلَدًا ﴿3﴾ وَإِنَّهُۥ كَانَ يَقُولُ سَفِيهُنَا عَلَى اَللَّهِ
شَطَطًا ﴿4﴾ وَإِنَّا ظَنَنَّا أَن لَّن تَقُولَ اَلْإِنسُ وَالْجِنُّ عَلَى اَللَّهِ كَذِبًا ﴿5﴾
وَإِنَّهُۥ كَانَ رِجَالٌ مِّنَ اَلْإِنسِ يَعُوذُونَ بِرِجَالٍ مِّنَ اَلْجِنِّ
فَزَادُوهُمْ رَهَقًا ﴿6﴾ وَإِنَّهُمْ ظَنُّوا كَمَا ظَنَنتُمْ أَن لَّن يَبْعَثَ اَللَّهُ
أَحَدًا ﴿7﴾ وَإِنَّا لَمَسْنَا اَلسَّمَآءَ فَوَجَدْنَٰهَا مُلِئَتْ حَرَسًا شَدِيدًا وَشُهُبًا ﴿8﴾
وَإِنَّا كُنَّا نَقْعُدُ مِنْهَا مَقَٰعِدَ لِلسَّمْعِ فَمَن يَسْتَمِعِ اِلْـَٰٔنَ يَجِدْ لَهُۥ
شِهَابًا رَّصَدًا ﴿9﴾ وَإِنَّا لَا نَدْرِي أَشَرٌّ اُرِيدَ بِمَن فِي اِلْأَرْضِ أَمْ أَرَادَ
بِهِمْ رَبُّهُمْ رَشَدًا ﴿10﴾ وَإِنَّا مِنَّا اَلصَّٰلِحُونَ وَمِنَّا دُونَ ذَٰلِكَ كُنَّا طَرَآئِقَ قِدَدًا ﴿11﴾
وَإِنَّا ظَنَنَّا أَن لَّن نُّعْجِزَ اَللَّهَ فِي اِلْأَرْضِ وَلَن نُّعْجِزَهُۥ هَرَبًا ﴿12﴾ وَإِنَّا لَمَّا سَمِعْنَا
اَلْهُدَىٰ ءَامَنَّا بِهِۦ فَمَن يُؤْمِنۢ بِرَبِّهِۦ فَلَا يَخَافُ بَخْسًا وَلَا رَهَقًا ﴿13﴾

Wannan Sura Itace Suratul Jinni

A Makka aka saukar da ita aya ishirin da takwas ce (28)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan sura ta ƙunshi haƙƙoki na Musulunci wanda Alƙur'am yayi furuci da ita. bisa harshen aljannu tareda fuskantarwowi wato taujihatu na Annabi SallAllahu alaihi wasallama).

1. Ka faɗa (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama ga mutane.) "an aiko izuwa gareni da wahayi daga Allah. haƙiƙa waɗansu aljannu (jinnin na sibina) sun saurari karatuna (a cikin.sallar asubane a bani Baɗni Nakhlata. wurine tsakanin Makka da ɗa'ifa) sukace (da mutanensu yayin da suka koma izuwa garesu,) "Mu Munji Alƙur'ani mai ban mamaki (a fusaha da yawan ma'ana da wanin wannan.)
2. "Da yake shiriya izuwa imani da wanin wannan sai muka bada gaskiya dashi, ba zamu sake shirkantawa Ubangijinmu da kowa ba (bayanyau.)
3. " Haƙiƙa lamarin girman Ubangijinmu ya girmama (ga buran abinda ake shirkantawa gareshi.) Bai taɓa riƙon macc wala ɗaba.
4. " Haƙiƙa lamarin jahilammu ya kasance yana faɗin magana da shishshigi ga Allah. (Shine dangana masa mace daɗa).
5. " Haƙiƙa mumuna zaton mutane da aljannu bazasu kwatantashi da wannan basuyi ƙarya da Allah ba. (hardai kuma ƙaryarsu ta bayyana).
6. "A haƙiƙa mazaje na mutane sun kasance suna neman tsari da mazaje na aljannu a (zamanin da suka sauka a gurin tsoro a cikin tafiyarsu, kowane mutum sai yace "ina neman tsari da shugaban wannan wuri daga wawayensa.) Sai mutane suka ƙarawa Aljannu shishshigi, (sukace sun shugabanci aljannu da mutane.)
7. Haƙiƙa su aljannu sunyi zato kamar daku ,mutane kuka zaci cewa Allah bazai tashi kowa bayan ya mutuba," (Aljannu sukace).
8. " Haƙiƙa mun nemi satarji daga sama sai muka sami an cikata da matsara masu ƙarfi da taurari masu ƙonewa wancanenka zamanin da aka aiko ma'aiki SallAllahu alaihi wasallama.
9. Haƙiƙa mun kasance gaban aiko shi muna zama gabanta don sauraro, to wanda yayi sauraro a yanzu ya saciji zai sami tauraro mai dako gareshi da aka dakatar dashi don a jefe shi dashi.
10. " Haƙiƙa mu bamu sani bashin sharri aka nufa (da rashin satar jinnan) ga wanda Yake cikin ƙasa? ko Ubangiji yanufi shiriyane dasu?
11. Haƙiƙa mu akwai salihai daga garemu bayan jin ƙur'ani, akwai daga garemu koma bayan wancanenka, (basalihai ba,(mun zama hanyoyi daban daban, (musulmai da kafirai).
12. " Haƙiƙa mumun sakankance cewa bazamu gajiyar da Allah a cikin ƙasa ba, bazamu tsere masa a guje ba.
13. " Haƙiƙa mu zamanin da mukaji Alƙur'ani mun bada gaskiya dashi, to wanda ya bada gaskiya da Ubangijinsa to bazaiji tsoron tauyewa (da hasanoninsa ba) wala gurmutsa (da ƙari a cikin saiy'arsa.)

وَأَنَّا مِنَّا ٱلْمُسْلِمُونَ وَمِنَّا ٱلْقَٰسِطُونَ فَمَنْ أَسْلَمَ فَأُوْلَٰٓئِكَ تَحَرَّوْا۟
رَشَدًا ﴿14﴾ وَأَمَّا ٱلْقَٰسِطُونَ فَكَانُوا۟ لِجَهَنَّمَ حَطَبًا ﴿15﴾ وَأَن لَّوِ
ٱسْتَقَٰمُوا۟ عَلَى ٱلطَّرِيقَةِ لَأَسْقَيْنَٰهُم مَّآءً غَدَقًا ﴿16﴾ لِّنَفْتِنَهُمْ
فِيهِ وَمَن يُعْرِضْ عَن ذِكْرِ رَبِّهِۦ نَسْلُكْهُ عَذَابًا صَعَدًا ﴿17﴾ * وَأَنَّ ثمن
ٱلْمَسَٰجِدَ لِلَّهِ فَلَا تَدْعُوا۟ مَعَ ٱللَّهِ أَحَدًا ﴿18﴾ وَإِنَّهُۥ لَمَّا قَامَ عَبْدُ ٱللَّهِ
يَدْعُوهُ كَادُوا۟ يَكُونُونَ عَلَيْهِ لِبَدًا ﴿19﴾ قَالَ إِنَّمَا أَدْعُوا۟ رَبِّي
وَلَآ أُشْرِكُ بِهِۦٓ أَحَدًا ﴿20﴾ قُلْ إِنِّيَ لَآ أَمْلِكُ لَكُمْ ضَرًّا وَلَا رَشَدًا ﴿21﴾
قُلْ إِنِّي لَن يُجِيرَنِي مِنَ ٱللَّهِ أَحَدٌ وَلَنْ أَجِدَ مِن دُونِهِۦ
مُلْتَحَدًا ﴿22﴾ إِلَّا بَلَٰغًا مِّنَ ٱللَّهِ وَرِسَٰلَٰتِهِۦ وَمَن يَعْصِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ
فَإِنَّ لَهُۥ نَارَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ﴿23﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا رَأَوْا۟
مَا يُوعَدُونَ فَسَيَعْلَمُونَ مَنْ أَضْعَفُ نَاصِرًا وَأَقَلُّ عَدَدًا ﴿24﴾ قُلْ إِنْ أَدْرِيَ
أَقَرِيبٌ مَّا تُوعَدُونَ أَمْ يَجْعَلُ لَهُۥ رَبِّيَ أَمَدًا ﴿25﴾ عَٰلِمُ ٱلْغَيْبِ فَلَا يُظْهِرُ
عَلَىٰ غَيْبِهِۦٓ أَحَدًا ﴿26﴾ إِلَّا مَنِ ٱرْتَضَىٰ مِن رَّسُولٍ فَإِنَّهُۥ يَسْلُكُ مِنۢ بَيْنِ يَدَيْهِ
وَمِنْ خَلْفِهِۦ رَصَدًا ﴿27﴾ لِّيَعْلَمَ أَن قَدْ أَبْلَغُوا۟ رِسَٰلَٰتِ رَبِّهِمْ
وَأَحَاطَ بِمَا لَدَيْهِمْ وَأَحْصَىٰ كُلَّ شَيْءٍ عَدَدًا ﴿28﴾

14. Haƙiƙa akwai musulmi daga garemu akwai kuma fanɗararru (saboda kafircinsu) to wanda ya musuluntа to waɗancanenka ne suka nufi shiriya. **15.** Amma fanɗararu to sun kasance gumagumen jahannama (da inna da innahun da innahu gurin nan goma sha biyu da kasran hamza ne ko fatahanta.) (ƊARIKATU JUNAIDIN ACIKIN ALƘUR'ANI)

16. Haƙiƙa lamarin, da sunyi daidai su waɗannan kafirai a kan ɗarika ta Musulunci, da mun shayar dasu ruwa mai yawa, (wancanenka bayan an ɗauke ruwane ga buransu shekara bakwai[1]. **17.** Don MU jarrabesu a cikinsa, (mu ganisa gode, kuma godiyarsu tabaiyana ga kowa.) Duka wanda ya bijire ga buran ambaton Ubangijinsa, ma shigar dashi azaba mai wuya.

18. Kuma haƙiƙa masallati na Allah ne, kadaku ,shirkanta tareda Allah a cikinta (tamfar da yahudu da Nasara suka kasance in sun shiga kanisosinsu ɗa bi'o'insu sai su shirkantada Allah.)

19. Kuma haƙiƙa al'amarin yayin da Abdullahi Babban bawan Allah (Sallallahu alaihi wasallama) ya tsaya yana bautawa Allah (a Baɗni Nahlata,) jinnin nasibina, sun kusa, su kasance labbatai (wato inasu cincirindo a cikin hawan shashi don matsatsa don kwaɗayi kan sauraron Alƙur'anı.) **20.** Manzon Allah yace (da kafirai, yayin da sukace dashi komo daga abinda kake kansa.) "ni ina bautawa Ubangijina ne bazan shirkanta kowa dashi a cikin bauta ba." (Malam yace:'Yan bidi'a basu fahinci ma'anar ibada da ma'anar soyayya da ban girma ba. saboda haka sai suka ɗauki girmama Annabawa da waliyai da ƙaunarsu a zuci Shine ibada garesu, basu fahinta ba. samun wannan a zuciyar mumini Shine ma'anar MUHAMMADUR RASULULLAH.) **21.** Cene " Haƙiƙa ni ban mallaki cuta gareku baban mallaki shiriya ba."

22. Cenc " Haƙiƙani ba wanda zai tserar da ni azabar Allah (in na saɓeshi.) Bazan sami mafaka ba har abada ba Allah ba. **23.** Ni ban mallaki komai basai ida aike da saƙonninsa, wanda ya saɓi Allah da manzanninsa bai bada gaskiya ba, haƙiƙa wutar jahannama ta tabbata garesu, masu dauwama a cikinta har abada.(Malam yace: Anan 'yan bidi'a sunyi kuskure babbada suka wajabta kore tsakaice-tsakaice tsakaninsu da Allah.) **24.** Bazasu gushe bakan kafircinsu harsu ga lokacin da ake musu azaba, wannene mafi rauni mafi ƙarancin mataimaka, (ba'alinsu ya faɗa ga ba'ali yaushe ne wannan alƙawarin?) **25.** Cene " Abinda ake muku alƙawari dashi (na azaba) makusancine, ko Ubangiji zaiyi masa lokaci (wanda ba wanda ya sanshi sai shi.) **26.** Masanin asirin take baya tsinkayar da kowa bisa gaibunsa. **27.** Sai wanda ya yarda dashi na daga jakada (ko waliyi) to haƙiƙa shi yana sanya masa dako nan gaba gareshi (manzon) da bayansa (harya iyar da saƙonsa.) (Inkarin ilhama ta auliya'u haramunne ijima'an. alƙur'an da hadisai sun zoda karamar waliyai, waɗanda bazasu ƙirgu ba, kuma abune wanda yake har izuwa yau izuwa gobe izuwa jibi izuwa tashin Alƙiyama.) **28.** Don Ubangiji ya bayyana (gareka) cewa haƙiƙa manzanni sun iyar da saƙonnin Ubangijinsu shi kuma ya kewaye da abinda yake gurinsu (wato yasan shi) kuma ya kewaye kowane abu da ƙirga.

1) Yan bidi a na wannan zamani namu suna musun ɗarikar Sufaye. suna cewa basu san asa-linta cikin .ALƘur'ani ba. wannan kawai makanta ce ta basira. in ba haka ba ita wannan ayata bayyana ƙarara cewa. ɗarriƙatul Islami. Wacce Shehu Mahalli ya fassara dariƙa da ita. itace Ɗarikati Junaidi Radiyallahu t'a'ala anhu; wacce ;aka samo ta daga aikin ahlissuffati].waɗanda aka saukar da ayoyi masu tarin yawa cikin bayanin kyakkyawan matsayinsu da tsarkakar halayensu bayan ayoyin tauhdi waɗanda suni Ɗariƙatul Islami Kamar yadda Sawi ya bayyana cewa aiki da ita ake nufi. wato bin ma'amuratu da nisantar manhiyyatu. wanda shi ake cewa takawa. wacce Itace darikar Sufaye. ba baɗı ba ragi. Abinda suke dashi na Hawarikul a-da-ti wato karamomi da ilimai na ilhamatu. natijar takawa ne. saboda haka sukace "ji tsoron Allah ka ga abin mamaki". Su'yan bidi'a da Allah yayi musu muwafuka ya danka musu siraɗal mustakima sun hau kan gwadabensa ta hanyar taƙawa wacce aka samo ta daga ma'aikin Allah Sal-lallahu alaihi wa sallama, da basuyi musun haƙiƙun LA ILAHA ILLALLAHU ba. waɗannan magangenu ijma'i ne na malaman Musulunci gabansu da bayansu. Allah yayi mana taufiki. yayi riko ga hannunmu gabaɗaya. amin. - Sanajiy -

73 سُورَةُ المُزَّمِّلِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ عِشْرُونَ ءَايَةً 20

بِسْمِ اِ۬للَّهِ اِ۬لرَّحْمَٰنِ اِ۬لرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا اَ۬لْمُزَّمِّلُ (1) قُمِ اِ۬ليْلَ إِلَّا قَلِيلاٗ (2) نِّصْفَهُۥٓ أَوُ اُ۟نقُصْ مِنْهُ قَلِيلاً (3)
أَوْ زِدْ عَلَيْهِ وَرَتِّلِ اِ۬لْقُرْءَانَ تَرْتِيلاً (4) إِنَّا سَنُلْقِے عَلَيْكَ قَوْلاٗ ثَقِيلاً (5)
إِنَّ نَاشِئَةَ اَ۬ليْلِ هِيَ أَشَدُّ وَطْـٔاٗ وَأَقْوَمُ قِيلاً (6) إِنَّ لَكَ فِے اِ۬لنَّهَارِ سَبْحاً
طَوِيلاٗ (7) وَاذْكُرِ اِ۪سْمَ رَبِّكَ وَتَبَتَّلِ إِلَيْهِ تَبْتِيلاٗ (8) رَّبُّ اُ۬لْمَشْرِقِ وَالْمَغْرِبِ
لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَاتَّخِذْهُ وَكِيلاٗ (9) وَاصْبِرْ عَلَيٰ مَا يَقُولُونَ وَاهْجُرْهُمْ
هَجْراٗ جَمِيلاٗ (10) وَذَرْنِے وَالْمُكَذِّبِينَ أُوْلِے اِ۬لنَّعْمَةِ وَمَهِّلْهُمْ قَلِيلاً (11)
إِنَّ لَدَيْنَآ أَنكَالاٗ وَجَحِيماٗ (12) وَطَعَاماٗ ذَا غُصَّةٖ وَعَذَاباً أَلِيماٗ (13)
يَوْمَ تَرْجُفُ اُ۬لْأَرْضُ وَالْجِبَالُ وَكَانَتِ اِ۬لْجِبَالُ كَثِيباٗ مَّهِيلاً (14)
إِنَّآ أَرْسَلْنَآ إِلَيْكُمْ رَسُولاٗ شَٰهِداً عَلَيْكُمْ كَمَآ أَرْسَلْنَآ إِلَيٰ فِرْعَوْنَ رَسُولاٗ (15)
فَعَصَيٰ فِرْعَوْنُ اُ۬لرَّسُولَ فَأَخَذْنَٰهُ أَخْذاٗ وَبِيلاٗ (16) فَكَيْفَ تَتَّقُونَ
إِن كَفَرْتُمْ يَوْماٗ يَجْعَلُ اُ۬لْوِلْدَٰنَ شِيباً (17) اِ۬لسَّمَآءُ مُنفَطِرُۢ بِهِۦ كَانَ وَعْدُهُۥ
مَفْعُولاً (18) إِنَّ هَٰذِهِۦ تَذْكِرَةٞ فَمَن شَآءَ اَ۪تَّخَذَ إِلَيٰ رَبِّهِۦ سَبِيلاً (19)

Wannan Sura Itace Suratul Muzammilu

A Makka aka saukar da ita aya goma sha takwas ce (18)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan sura ta tattara bisa shirye shirye na ma'aikin Allah SallAllahu alaihi wasallama, saboda ƙarfafa jikinsa da ransa, harya sami iko bisa ɗaukan risala, sannan umarninsa da haƙuri a kan cutar mushurikai tareda firgitarwa garesu da shirye shirye ga shugaban kiran Musulunci (Sallallahu alaihi wasallama).

1. Ya wannan Annabi mai lulluɓa da tufofinsa (yayin zuwan wahayi gareshi don tsoronsa saboda kwarjininsa) kayi salla dukan dare sai kaɗan.
2. Rabinsa ko ka rage wani abu ƙanƙani daga nusifin nan izuwa sulusi.
3. Koka ƙara a kansa izuwa sulusaini, ka kyauta ta karatun al-ƙur'ani kyautatawa.
4. Haƙiƙa MUda sannu zamu jefa maka magana mai nauyi (shine alƙur'ani, mai kwarjini, don abin da yake cikinsa na daga kallafe-kallafe.)
5. Haƙiƙa tsaiwar dare Itace tafi dacewa a bisa fahintar alƙur'ani, Itace tafi baiyanar magana.
6. Haƙiƙa da rana kana da tasarrufi a cikin shagulgulanka (bazaka samu sararin karatun alƙur'ani a cikinsa ba.)
7. Ka ambaci sunan Ubangijinka a cikin farkon karatunka, ka yanku izuwa ibadodinsa (wato ka dauwama a kan ambaton Ubangijinka da daddare ko da rana a kowace fuska, wato tasbihi ne tahmidi ne da makamancin wannan Sawi Malam yace:Zikirai waɗanda waliyai suka shirya Anfarasu da Zikiril Kariri da Ismi Sadri wato Zikirin kakari da sauran irinsu suna shiga cikin wannan wanahwu zalika.)
8. Shine Ubangijin gabas da yamma ba abin bautawa saishi, ka riƙeshi abin dogara.
9. Ka daure a bisa abinda kafiran Makka suke faɗa maka, ka ƙaurace musu ƙauracewa kyakkyawa (wanda ba raki cikinsa, wannan gaban umarni da yaƙinsu ne.)
10. Barni tareda masu ƙaryatashi (sune gingin-gingin ɗin ƙuraishawa,) ma'abota more daɗin duniya, kai masu jinkiri kaɗan (aka kashesu bayan zamani kaɗan a badar.)
11. Haƙiƙa akwai maruruwa a garemu da wuta mai ƙonewa.
12. Da abinci mai maƙare maƙogwaro (Shine zaƙum kamar da aka samo a cikin littafi MIFTAHU FALAHI na ibn Shehu Ada'illahi ƙayacc ta wuta, wacce bata sauka, bata fita) da azaba mai raɗaɗi.
13. Ranar da ƙasa take girgiza da duwarwatsu ta zamo rairayi mai tisgawa.
14. Haƙiƙa mu mun aiko manzo izuwa gareku (yaku mutanen Makka shine Annabi Sallallahu alaihi wasallama,) mai shaidawa gareku (ranar alƙiyama da abinda ya faru gareku na saɓo,) tamfar cla muka aiko manzo izuwa Firauna (shine Annabi Musa Alaihissalamu.)

15/16. Sai Fir'aunu ya saɓawa wannan manzon (Annabi Musa Alaihissalamu,) Ubangiji ya damƙeshi damƙa mai tsanani.

17/18. Ta yaya zakuji tsoron (azaba mai girma?) inkun kafirce (a duniya,) rana wanda yake sanya ƙananan yara ,suyi furfura, sama mai kyerkecewace, (saboda wancananka rana saboda wuyarsa,) alƙawarin Ubangiji abin aikatawane (ba makawa zaizo.)

19. Waɗannan ayoyi gargaɗine, wanda yaga dama ya riƙi hanya izuwa Ubangijinsa (ta imani da ɗa'a).

ربع

* إِنَّ رَبَّكَ يَعْلَمُ أَنَّكَ تَقُومُ أَدْنَىٰ مِن ثُلُثَيِ اِ۬ليْلِ وَنِصْفِهِۦ وَثُلُثِهِۦ وَطَآئِفَةٌ مِّنَ
اَ۬لذِينَ مَعَكَ وَاللَّهُ يُقَدِّرُ اُ۬ليْلَ وَالنَّهَارَ عَلِمَ أَن لَّن تُحْصُوهُ فَتَابَ عَلَيْكُمْ
فَاقْرَءُواْ مَا تَيَسَّرَ مِنَ اَ۬لْقُرْءَانِ عَلِمَ أَن سَيَكُونُ مِنكُم مَّرْضَىٰ وَءَاخَرُونَ
يَضْرِبُونَ فِي اِ۬لْأَرْضِ يَبْتَغُونَ مِن فَضْلِ اِ۬للَّهِ وَءَاخَرُونَ يُقَاتِلُونَ فِي سَبِيلِ اِ۬للَّهِ
فَاقْرَءُواْ مَا تَيَسَّرَ مِنْهُ وَأَقِيمُواْ اُ۬لصَّلَوٰةَ وَءَاتُواْ اُ۬لزَّكَوٰةَ وَأَقْرِضُواْ اُ۬للَّهَ
قَرْضاً حَسَناً وَمَا تُقَدِّمُواْ لِأَنفُسِكُم مِّنْ خَيْرٍ تَجِدُوهُ عِندَ اَ۬للَّهِ
هُوَ خَيْراً وَأَعْظَمَ أَجْراً وَاسْتَغْفِرُواْ اُ۬للَّهَ إِنَّ اَ۬للَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿20﴾

74 سُورَةُ الْمُدَّثِّرِ مَكِّيَّةٌ
وَهِيَ سِتٌّ وَخَمْسُونَ ءَايَةً 56

بِسْمِ اِ۬للَّهِ اِ۬لرَّحْمَٰنِ اِ۬لرَّحِيمِ

يَٰٓأَيُّهَا اَ۬لْمُدَّثِّرُ ﴿1﴾ قُمْ فَأَنذِرْ ﴿2﴾ وَرَبَّكَ فَكَبِّرْ ﴿3﴾ وَثِيَابَكَ فَطَهِّرْ ﴿4﴾
وَالرُّجْزَ فَاهْجُرْ ﴿5﴾ وَلَا تَمْنُن تَسْتَكْثِرُ ﴿6﴾ وَلِرَبِّكَ فَاصْبِرْ ﴿7﴾ فَإِذَا نُقِرَ
فِي اِ۬لنَّاقُورِ ﴿8﴾ فَذَٰلِكَ يَوْمَئِذٍ يَوْمٌ عَسِيرٌ ﴿9﴾ عَلَى اَ۬لْكٰفِرِينَ غَيْرُ يَسِيرٍ ﴿10﴾ ذَرْنِي وَمَنْ
خَلَقْتُ وَحِيداً ﴿11﴾ وَجَعَلْتُ لَهُۥ مَالًا مَّمْدُوداً ﴿12﴾ وَبَنِينَ شُهُوداً ﴿13﴾ وَمَهَّدتُّ لَهُۥ
تَمْهِيداً ﴿14﴾ ثُمَّ يَطْمَعُ أَنْ أَزِيدَ ﴿15﴾ كَلَّا إِنَّهُۥ كَانَ لِءَايَٰتِنَا عَنِيداً ﴿16﴾ سَأُرْهِقُهُۥ صَعُوداً ﴿17﴾

(WANCANANKU SAUWAƘEWANE DAGA ALLAH DA .JINƘAI)

20. Ubangijinka yasan kai kana tsaiwa mafi ƙaranci daga sulusaini na dare da nusfinsa da sulusinsa da jama'a da yawa waɗanda suka bada gaskiya taredakai (na daga sahabbai, suma suna yin haka don kwaikwayo ga ma'aikin Allah (SallAllahu alaihi wasallama akwai daga garesu wanda bai san nawa ya sallata daga dare ba ko nawane daga dare ya ragu saiya zama yana sallar dukkan daren don ihtiyaɗi, suka dinga tsaiwa har dugadugan.su suka dinga kumbura shekara guda, ko mafi yawa daga haka, sai Ubangiji ya ɦaffafe musu yace,} Ubangiji ya kewaye dare da rana, yasan cewa bazaku kewaye tsaiwar dare ba a cikin cewa abinda ya wajaba saidai inkun tsaya a dukkan daren. (Wancanenku zai wahalar daku,) sai Ubangiji ya karɓi tubanku (yakoma daku ,izuwa sauwaƙewa,) to ku karanta abinda ya sauwaƙa na alƙur'ani (a cikin salloli, ku sallaci abinda ya sauwaƙa' na daga alƙur'ani,) yasan haƙiƙa za a sami marasa lafiya daga gareku da waɗansu ,sunayin tafiya a cikin ƙasa suna neman falalar Allah (na arziki da ciniki ko waninsa,) waɗansu kuma suna yaƙi cikin inganta addinin Allah, (abin nan da aka ambata .ai wahalar dasu a tsayuwar dare aka sawwaƙe musu abinda ya sauwaƙa daga gareshi sannan aka shafe shi da salawatul hamsi,) toku karanta abinda ya sauwaƙa daga gareshi. ku tsaida salla farilla ku bada zakka, ku rantawa Allah (daga abinda kuke ciyarwa ba a wajibi bana daga dukiyarku) rance kyakkyawa (kuyi alheri da dukiya a cikin daɗin rai) duk abinda kuke gabatarwa ga kawukanku na alheri zaku sameshi nan ga Ubangiji. shi abinda kuka gabatar yafi amfani mafi girma a wajen lada. ku nemi gafarar Allah. haƙiƙa Ubangiji mai gafara ne mai jinƙai (ga muminai.)

Wannan Sura Itace Suratul Mudassiru

A Makka aka saukar da ita aya hamsin da biyar ce (55)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

Wannan sura ta ɗauki Irshabodi ga ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wasallama, da yake buƙata gareshi a cikin kiransa, sannan ban tsoro daga shuwagabannin Mushurikanci da Jahannama. Wannan Sura data gabata sun (kamanci juna, ta farko a cikin tanadin Annabi Makirayi, ta biyu kuma Shiryar dashi abinda zai kaishi yaci nasara.

(FUSKANCE-FUSKANCE GA MA'AIKI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

1. Ya wannan (Annabi Sallallahu alaihi wasallama) mai lulluɓi da tufatinsa (yayin saukar wahayi gareshi). **2.** Tashi tsaye ka gargaɗar (da mutanen Makka in basu bada gaskiya ba.) **3.** Ka girmama ubangijinka (ga barin shirkar nan ta mushurkai.) **4.** Ka tsarkake tufafinka (ga buran ƙazanta koka ɗageta, saɓanin yadda Larabawa. Suke jan ta a ƙasa don girman kai, da yawa najasa zata sameta.) **5.** Ka dauwama kan ƙauracewa gumaka. **6.** Kadaka bada abu donka nemi mafi yawa daga gareshi. (wannan keɓantacce ne ga Annabi Sallallahu alaihi wasallama saboda shi abin umarnine da mafi kyan fa'idodi.) **7.** Ka daure ga Ubangijinka a kan umarni da hane-hane. **8.** Idan akayi busa a cikin ƙaho busa ta biyu. **9.** Wancanenka ranar busar nan ranace mai tsanani. **10.** A bisa kafirai ba mai sauƙine ba.

(ABINDA SHUWAGABANNIN MUSHURKANCI SUKE GAMUWA DASHI)

11. Barni da wanda na halicceshi shi kaɗai (ba iyali ba dukiya Shine Walidu ɗan Mugira ALMAKHZUMI.) **12.** Na sanya masa dukiya abin miƙawa (na hatsi da hantsotsi da ciniki.) **13.** Da 'ya'yaye (guda goma) masu halattar taruka. **14.** Na yalwata masa (a rayuwa da abinci da 'ya'yaye) yalwatawa. **15.** Sannan yana tsammanin in ƙara masa. **16.** Kai bazan ƙara masa a kan wannan ba, haƙiƙa shiya kasance mai taurin kai ga ayoyinmu (alƙur'ani.)

17. Da sannu zan ɗora masa wahala ta azaba, (Shine hawa dutsen wuta sannan yayiwo dake a cikin wuta har abada.)

إِنَّهُۥ فَكَّرَ وَقَدَّرَ ﴿18﴾ فَقُتِلَ كَيْفَ قَدَّرَ ﴿19﴾ ثُمَّ قُتِلَ كَيْفَ قَدَّرَ ﴿20﴾ ثُمَّ نَظَرَ ﴿21﴾
ثُمَّ عَبَسَ وَبَسَرَ ﴿22﴾ ثُمَّ أَدْبَرَ وَاسْتَكْبَرَ ﴿23﴾ فَقَالَ إِنْ هَٰذَا إِلَّا سِحْرٌ يُوثَرُ ﴿24﴾
إِنْ هَٰذَا إِلَّا قَوْلُ الْبَشَرِ ﴿25﴾ سَأُصْلِيهِ سَقَرَ ﴿26﴾ وَمَا أَدْرِيكَ مَا سَقَرُ ﴿27﴾
لَا تُبْقِي وَلَا تَذَرُ ﴿28﴾ لَوَّاحَةٌ لِّلْبَشَرِ ﴿29﴾ عَلَيْهَا تِسْعَةَ عَشَرَ ﴿30﴾
ثمن
* وَمَا جَعَلْنَا أَصْحَٰبَ النَّارِ إِلَّا مَلَٰٓئِكَةً وَمَا جَعَلْنَا عِدَّتَهُمْ إِلَّا فِتْنَةً
لِّلَّذِينَ كَفَرُوا لِيَسْتَيْقِنَ الَّذِينَ أُوتُوا الْكِتَٰبَ وَيَزْدَادَ الَّذِينَ ءَامَنُوا إِيمَٰنًا
وَلَا يَرْتَابَ الَّذِينَ أُوتُوا الْكِتَٰبَ وَالْمُومِنُونَ وَلِيَقُولَ الَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٌ
وَالْكَٰفِرُونَ مَاذَا أَرَادَ اللَّهُ بِهَٰذَا مَثَلًا كَذَٰلِكَ يُضِلُّ اللَّهُ مَن يَشَاءُ
وَيَهْدِي مَن يَشَاءُ وَمَا يَعْلَمُ جُنُودَ رَبِّكَ إِلَّا هُوَ وَمَا هِيَ إِلَّا ذِكْرَىٰ
لِلْبَشَرِ ﴿31﴾ كَلَّا وَالْقَمَرِ ﴿32﴾ وَاليْلِ إِذْ أَدْبَرَ ﴿33﴾ وَالصُّبْحِ إِذَا أَسْفَرَ ﴿34﴾
إِنَّهَا لَإِحْدَى الْكُبَرِ ﴿35﴾ نَذِيرًا لِّلْبَشَرِ ﴿36﴾ لِمَن شَاءَ مِنكُمُ أَن يَتَقَدَّمَ
أَوْ يَتَأَخَّرَ ﴿37﴾ كُلُّ نَفْسٍ بِمَا كَسَبَتْ رَهِينَةٌ ﴿38﴾ إِلَّا أَصْحَٰبَ الْيَمِينِ ﴿39﴾
فِي جَنَّٰتٍ يَتَسَاءَلُونَ ﴿40﴾ عَنِ الْمُجْرِمِينَ ﴿41﴾ مَا سَلَكَكُمْ فِي سَقَرَ ﴿42﴾ قَالُوا
لَمْ نَكُ مِنَ الْمُصَلِّينَ ﴿43﴾ وَلَمْ نَكُ نُطْعِمُ الْمِسْكِينَ ﴿44﴾ وَكُنَّا نَخُوضُ مَعَ
الْخَائِضِينَ ﴿45﴾ وَكُنَّا نُكَذِّبُ بِيَوْمِ الدِّينِ ﴿46﴾ حَتَّىٰ أَتَىٰنَا الْيَقِينُ ﴿47﴾

18. Saboda yayi tunani (cikin abinda zai faɗa na alƙur'ani wanda yaji (shi daga manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama) ya gwargwada (kansa a cikin haka.)
19. An tsine masa irin yadda duk ya gwargwada.
20. Sannan an sake tsine masa al-barka irin yadda duk ya gwargwada.
21. Sannan ya dubi (fuskokin mutanensa ko yayi duba cikin abinda zaiyi sûka dashi a cikin ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wasallama).
22. Sannan ya daure fuskarsa (don ƙuncin abinda zai faɗa ya murtuketa).
23. Sannan ya juya baya a cikin imani, yayi girman kai (ga buran bin Annabi Sallallahu alaihi wasallama).
24. Yace (a cikin abinda yazo dashi) "bai kasance basai tsafi da ake ruwaitowa."
25. "Wannan bai kasance basai faɗin mutum."
26. Da sannu zan shigar dashi Saƙaru (wato wutar jahannama).
27. Wane abune ya sanar dakai Mcnene Saƙaru?
28. Bata wanzarwa bata ragewa (da komai na jijiya ko nama. face saita halakar dashi.)
29. Mai ƙandarewa ga zihirin fata.
30. Akwai Mala'ika goma sha tara (matsaranta. sai ba'alin kafirai yace, alhali ƙaƙƙarfane mai tsananin faɗa. yace shi zai isar musu su kuma su tare biyu, sai Ubangiji yace).
31. "Bamu sanya 'yan wutan nan ba. sai Mala'iku (waɗanda ba a iya karawa dasu.) bamu sanya ƙirgarsu basai don fitina garesu, sai waɗanda aka baSU littafi (Yahudawa. SU sakankance (da gaskiyar Annabi domin adadin ya dace da abinda ke cikin littafinsu.) Waɗanda suka bada gaskiya su ƙara imani (don wannan dacewar) kada waɗanda aka basu littafi da Muminai suyi kokonto (a cikin Mala'ikun) saboda waɗanda munafinci, yake cikin Zukatansu suce, "me Allah Yake nufi da wannan a misali). Kamar yadda ya ɓatar da masu musun Wannan adadi, ya shiryi masu gasgatashi, yake ɓatar da wanda yaga dama, yakc shiriyar wanda yaga dama, babu wanda yasan rundunar Ubangijinka na Mala'iku a cikin ƙarfinsu da taimakonsu sai Allah kawai. Ita Saƙara bata kasance ba. face gargaɗi ne ga talikai.

(WUTAR SAƘARA DA WANDA YAKE CIKINTA)

32. (To jama a) Allah ya rantse da wata da dare idan ya bada baya.
33. Ya rantse da dare lokacin daya bada baya.
34. Ya rantse da asubahi idan ya fice.
35. Haƙiƙa Saƙara ɗayan manyan masifofice gingin-gingin.
36. Halin kasancewarta mai gargaɗi ga talikai.
37. Ga wanda yaga dama gareku yagabata (izuwa alheri ko aljanna da imani) ko ya jinkirta (izuwa sharri ko wuta da kafirci.)
38. Dukkan gudan rai ta mutum jinginanniyace da abinda ta aikata na wuta.
39. Sai 'yan dama (sune muminai. tosu masu tsirane daga gareta.)
40. .Suna cikin aljannatai, suna tam-baya (tsakaninsu game da masu laifi, suna cewa bayan fitar da mai tauhidi daga wuta.)
41. "Me ya shigar daku ,cikin Sakara?"
42. Sai sukace "Bamu kasance cikin ma.su salla ba."
43. "Bamu kasance muna cida miskini ba."
44. "Mun kasance muna kutsawa tareda masu kutsawa (a cikin ɓarna.")
45. "Mun ƙasance muna ƙaryatawa da tashin alƙiyama da sakamako."
46. "Har mutuwa tazo mana."
47. Ceton masu ceto bazata samesu ba (na daga Annabawa da Mala'ikuda salihai.)

فَمَا تَنفَعُهُمْ شَفَاعَةُ الشَّافِعِينَ ﴿48﴾ فَمَا لَهُمْ عَنِ التَّذْكِرَةِ مُعْرِضِينَ ﴿49﴾ كَأَنَّهُمْ
حُمُرٌ مُّسْتَنفَرَةٌ ﴿50﴾ فَرَّتْ مِن قَسْوَرَةٍ ﴿51﴾ بَلْ يُرِيدُ كُلُّ امْرِئٍ مِّنْهُمْ أَن يُؤْتَىٰ صُحُفًا
مُّنَشَّرَةً ﴿52﴾ كَلَّا بَل لَّا يَخَافُونَ الْآخِرَةَ ﴿53﴾ كَلَّا إِنَّهُ تَذْكِرَةٌ ﴿54﴾ فَمَن شَاءَ
ذَكَرَهُ ﴿55﴾ وَمَا تَذْكُرُونَ إِلَّا أَن يَشَاءَ اللَّهُ هُوَ أَهْلُ التَّقْوَىٰ وَأَهْلُ الْمَغْفِرَةِ ﴿56﴾

75 سُورَةُ الْقِيَامَةِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ تِسْعٌ وَثَلَاثُونَ آيَةً 39

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

ربع

* لَا أُقْسِمُ بِيَوْمِ الْقِيَامَةِ ﴿1﴾ وَلَا أُقْسِمُ بِالنَّفْسِ اللَّوَّامَةِ ﴿2﴾ أَيَحْسِبُ الْإِنسَانُ
أَلَّن نَّجْمَعَ عِظَامَهُ ﴿3﴾ بَلَىٰ قَادِرِينَ عَلَىٰ أَن نُّسَوِّيَ بَنَانَهُ ﴿4﴾ بَلْ يُرِيدُ الْإِنسَانُ
لِيَفْجُرَ أَمَامَهُ ﴿5﴾ يَسْأَلُ أَيَّانَ يَوْمُ الْقِيَامَةِ ﴿6﴾ فَإِذَا بَرَقَ الْبَصَرُ ﴿7﴾
وَخَسَفَ الْقَمَرُ ﴿8﴾ وَجُمِعَ الشَّمْسُ وَالْقَمَرُ ﴿9﴾ يَقُولُ الْإِنسَانُ يَوْمَئِذٍ أَيْنَ
الْمَفَرُّ ﴿10﴾ كَلَّا لَا وَزَرَ ﴿11﴾ إِلَىٰ رَبِّكَ يَوْمَئِذٍ الْمُسْتَقَرُّ ﴿12﴾ يُنَبَّأُ الْإِنسَانُ
يَوْمَئِذٍ بِمَا قَدَّمَ وَأَخَّرَ ﴿13﴾ بَلِ الْإِنسَانُ عَلَىٰ نَفْسِهِ بَصِيرَةٌ ﴿14﴾ وَلَوْ أَلْقَىٰ
مَعَاذِيرَهُ ﴿15﴾ لَا تُحَرِّكْ بِهِ لِسَانَكَ لِتَعْجَلَ بِهِ إِنَّ عَلَيْنَا جَمْعَهُ وَقُرْءَانَهُ ﴿16﴾
فَإِذَا قَرَأْنَاهُ فَاتَّبِعْ قُرْءَانَهُ ﴿17﴾ ثُمَّ إِنَّ عَلَيْنَا بَيَانَهُ ﴿18﴾

48. Shin meya same sune suke bijirewa ga buran gargaɗi?
49. Kai kacesu Jakunane na jeji.
50. Data gujewa zaki a guje.
51. Kai dai kowane mutum daga cikinsu yanaso a bashi littattafai ababan daidaitawa (daga Allah da bin Annabi tamfar da sukace bazasu bada gaskiya dashi ba har saiya saukar da littafi da zasu karantashi).
52. Hir! daga abin nan da kuka nema. Kaiku dai bakwa tsoron Lahira.
53. To shi alƙur'ani dai gargaɗi ne.
54. Haƙiƙa alƙurani gargaɗine wanda yaga dama ya karantashi ko ya wa'azantu dashi.
55. Bakwa wa'zantuwa dai sai in Allah yaga dama, Ubangijine ya cancanci a tsoroceshi, Shine mai yin gafara (ga wanda yaji tsoronsa.)

Wannan Sura Itace Suratul Ƙaiyimati

a Makka aka saukar da ita aya talatin da tara ce (39)

Ina tarawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

wannan Sura tana magana a kan Ranar Alƙiyama da Kafa dalili a kansa da Sifarsa da bayanın Tsarmakatansa da Zancen fitar Rai da Ambaton ƙarkon Halitta.

(RANAR ALƘIYAMA DA ABINDA YAKE CIKINSA)

1. Ina rantsuwa da ranar alƙiyama,(da abinda Yake cikinta.)
2. Kuma ina rantsuwa dakai mai yawan zargin mai ita (koda tayi ƙoƙari cikin kyautata aiki. Abinda aka rantse a kansa shafaffene shine Wallahi za a tasheku.)
3. Donme kafiri zai zaci bazamu tara ƙasusuwansu ba (saboda tashi da rayawa?)
4. A'a zamu tarata, muna gwanaye a kan tara ta, gwanaye a kanmu daidaita 'yan yatsunsa, (wato MU maida ƙasusuwanta tamkar data kasance tareda ƙanƙantarta, yaya mai girma kuma? Min babi aula.)
5. Bari! mutum yana nufin yayi fajirci a gaban ranar alƙiyama, (wato yayi ƙarya).
6. Yana tambaya yaushe ne ranar alƙiyama? (Tambaya irin ta izgili da ƙaryatawa.)
7. To idan gani ya ƙafe (saboda abinda yagani na abinda ya ƙaryata dashi).
8. Hasken wata ya duhunta.
9. To a wannan rana ake tara rana da wata (suka hudo daga yamma, ko haskensu ya tashi, wannan a ranar Alƙiyama kenan).
10. Mutum zai dinga cewa a wannan rana ina maguda?
11. Ahir! ga buran neman gudu ba mataka daza a tsira dashi.
12. Komawar halitta a wannan rana izuwa Ubangijinkane, (ayi musu sakamako).
13. Ana baiwa mutum labari da abinda ya gabatar da abinda ya jinkirtar (ƙarkon aikinsa da ƙarshensa a wannan rana.)
14. Bari! shi mutum malamine a bisa kansa (gaɓuɓɓansa zasuyi furuci da aikinsa ba makawa dagayi masa sakamako.)
15. Kodazai zoda hanzare-hanzarensa (baza a karɓa daga gareshi ba.) (Sai Ubangiji yace da Annabi Sallallahu alaihi wasallama).
16. "Kadaka motsa harshenka da Alƙur'ani gaban gamawar Jibrilu daga karatunsa, don kai garaje dashi (tsoron kada ya kubuce maka,) haƙiƙa tara shi a ƙirjinka yana kanmu da karantashi a (kan harshenka.)
17. Idan mun karantashi gareka (da karatun Jibrilu,) to bi karatunsa (manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama ya kasance yana sauraro sannan ya karanta.)
18. Sannan yi maka bayaninsa, yana garemu (mu fahimtar makashi munasaba tsakanin wannan aya da wacce take gabanta, Shine cewa wancanenka ta ƙunshi bijirewa ga buran ayoyin Allah, wannan kuwa ta ƙunshi gaggautawa izuwa haddaceta.

كَلَّا بَلْ تُحِبُّونَ اَ۬لْعَاجِلَةَ (19) وَتَذَرُونَ اَ۬لْأٓخِرَةَ (20) وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ
نَّاضِرَةٌ (21) إِلَىٰ رَبِّهَا نَاظِرَةٌ (22) وَوُجُوهٌ يَوْمَئِذِۢ بَاسِرَةٌ (23) تَظُنُّ أَن يُّفْعَلَ
بِهَا فَاقِرَةٌ (24) كَلَّا إِذَا بَلَغَتِ اِ۬لتَّرَاقِيَ (25) وَقِيلَ مَن رَّاقٍ (26) وَظَنَّ أَنَّهُ
اُ۬لْفِرَاقُ (27) وَالْتَفَّتِ اِ۬لسَّاقُ بِالسَّاقِ (28) إِلَىٰ رَبِّكَ يَوْمَئِذٍ اِ۬لْمَسَاقُ (29)
فَلَا صَدَّقَ وَلَا صَلَّىٰ (30) وَلَٰكِن كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰ (31) ثُمَّ ذَهَبَ إِلَىٰ أَهْلِهِۦ يَتَمَطَّىٰ (32)
أَوْلَىٰ لَكَ فَأَوْلَىٰ (33) ثُمَّ أَوْلَىٰ لَكَ فَأَوْلَىٰ (34) أَيَحْسِبُ اُ۬لْإِنسَانُ أَن يُّتْرَكَ سُدًى (35)
أَلَمْ يَكُ نُطْفَةً مِّن مَّنِيٍّ تُمْنَىٰ (36) ثُمَّ كَانَ عَلَقَةً فَخَلَقَ فَسَوَّىٰ (37) فَجَعَلَ مِنْهُ
اُ۬لزَّوْجَيْنِ اِ۬لذَّكَرَ وَالْأُنثَىٰ (38) أَلَيْسَ ذَٰلِكَ بِقَٰدِرٍ عَلَىٰ أَن يُّحْيِۦ اَ۬لْمَوْتَىٰ (39)

76 سُورَةُ الْإِنسَانِ مَدَنِيَّةٌ

وَهِيَ إِحْدَىٰ وَثَلَاثُونَ ءَايَةً 31

بِسْمِ اِ۬للَّهِ اِ۬لرَّحْمَٰنِ اِ۬لرَّحِيمِ

* هَلْ أَتَىٰ عَلَى اَ۬لْإِنسَانِ حِينٌ مِّنَ اَ۬لدَّهْرِ لَمْ يَكُن شَيْـًٔا مَّذْكُورًا (1) إِنَّا خَلَقْنَا ثمن
اَ۬لْإِنسَانَ مِن نُّطْفَةٍ أَمْشَاجٍ نَّبْتَلِيهِ فَجَعَلْنَٰهُ سَمِيعًۢا بَصِيرًا (2) إِنَّا هَدَيْنَٰهُ
اُ۬لسَّبِيلَ إِمَّا شَاكِرًا وَإِمَّا كَفُورًا (3) إِنَّا أَعْتَدْنَا لِلْكَٰفِرِينَ سَلَٰسِلَا وَأَغْلَٰلًا
وَسَعِيرًا (4) إِنَّ اَ۬لْأَبْرَارَ يَشْرَبُونَ مِن كَأْسٍ كَانَ مِزَاجُهَا كَافُورًا (5)

19. Bari! (Ku jama'a) kuna son magaggauciya (Itace duniya).
20. Kuna barin ranar Lahira (bakwa yin aiki saboda ita.)
21. Fuskoki a wannan rana mani'imtane.
22. Masu dubane izuwa Ubangijinsu.
23. Da fuskoki a wannan rana wacce tayi murtuk.
24. Ta tabbata za ayi mata masifa, (wato a karya tsatsonta.)

(MUNTUM YAYIN MUTUWARSA DAYAYIN FARA HALITTARSA)

25. To jama'a! Zamanin da rai ta isa mundayen wuya.
26. Wanda yake daura dashi yace "Waye mai tawaida?".
27. Ya tabbatar cewashi rabuwa zaiyi da duniya.
28. Dayan makangyamarsa ta haɗuda ɗaya.
29. Izuwa Ubangijinkane korashi ta tabbata a wannan rana.
30. To shi mutum bai gasgata Allah ba baiyi salla ba.
31. Saidai ya ƙaryata alƙur'ani ya juya ga buran imani.
32. Sannan ya tafi yana taƙama izuwa iyalinsa (don jiji da kai).
33. Abinda kake ƙi yabika, to Shine yafi dacewa da kai.
34. Sannan abinda kake ƙi yabika, to Shine yafi dacewa da kai.
35. Me yasa mutum yake zaton a barshi sasakai (baza ayi masa taklifi da shari'u ba, ya daina zaton haka.)
36. Shin bai kasance ɗigon majina na maniyi da ake zubawa a cikin mahaifa ba?
37. Sannan ya kasance gudan jini. Allah ya halicci mutum daga shi, ya daidaita gaɓuɓɓansa.
38. Ya halicci nau'i biyu dagashi wannan ɗigon majina, wanda ya zama gudan jini, sannan tsokar nama, aka halicci nau'i biyu:namiji da mace (sukan tattara wani yayi, wani yayi kuma kowanne ya waru daga ɗan'uwansa.)
39. Shin mai aikata (wannan abubuwa ba mai iko bane bisa ya raya ƙasusuwa (bayan mutuwa? Lallai mai ikone.)

Wannan Sura Itace Suratul Insanu

a Makka aka saukar da ita aya talatin da ɗayace (31)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

1. Haƙiƙa wani lokuci na zamani yazo bisa mutum (Annabi Adamu Alaihissalamu Shine shekara 40) bai kasance abin ambato ba (a cikinsa, ya kasance abin surantawa daga yunɓu.)
2. Haƙiƙa mun halicci mutum, (wato jinsin mutum) daga majinar maniyi macuɗanyi ruwan namji dana mace, muna jarrabashi da taklifi, (wato muna masu nufin jarrabarsa a lokacin daya dace,) saboda haka muka sanyashi mai ji mai gani.
3. Haƙiƙa mun baiyana masa hanya tashiriya (saboda aiko manzanni,) imina mai godiya, (wato mumini) wa imma mai kafircewa (wato kafiri.)
4. Haƙiƙa mu mun tanadi sarƙoƙi (ana jansu da ita a cikin wuta,) da ƙuƙumai (a wuyayinsu da ake ɗaure sarƙoƙin nan,) da wuta abar hurawa.

(MANAGARTA DA AIYUKANSU DA SAKAMAKONSU)

5. Haƙiƙa managarta suna sha daga gidauniyar giya ta aljanna, abin tsarmawarta ya kasance kafurne.

عَيْناٗ يَشْرَبُ بِهَا عِبَادُ اُ۬للَّهِ يُفَجِّرُونَهَا تَفْجِيراٗ ﴿6﴾ يُوفُونَ بِالنَّذْرِ وَيَخَافُونَ
يَوْماٗ كَانَ شَرُّهُۥ مُسْتَطِيراٗ ﴿7﴾ وَيُطْعِمُونَ اَ۬لطَّعَامَ عَلَيٰ حُبِّهِۦ مِسْكِيناٗ وَيَتِيماٗ
وَأَسِيراً ﴿8﴾ إِنَّمَا نُطْعِمُكُمْ لِوَجْهِ اِ۬للَّهِ لَا نُرِيدُ مِنكُمْ جَزَآءٗ وَلَا شُكُوراً ﴿9﴾ إِنَّا نَخَافُ
مِن رَّبِّنَا يَوْماً عَبُوساٗ قَمْطَرِيراٗ ﴿10﴾ فَوَقَيٰهُمُ اُ۬للَّهُ شَرَّ ذَٰلِكَ اَ۬لْيَوْمِ وَلَقَّيٰهُمْ
نَضْرَةٗ وَسُرُوراٗ ﴿11﴾ وَجَزَيٰهُم بِمَا صَبَرُواْ جَنَّةٗ وَحَرِيراٗ ﴿12﴾ مُّتَّكِـِٔينَ
فِيهَا عَلَي اَ۬لْأَرَآئِكِ لَا يَرَوْنَ فِيهَا شَمْساٗ وَلَا زَمْهَرِيراٗ ﴿13﴾ وَدَانِيَةً عَلَيْهِمْ
ظِلَٰلُهَا وَذُلِّلَتْ قُطُوفُهَا تَذْلِيلاٗ ﴿14﴾ وَيُطَافُ عَلَيْهِم بِـَٔانِيَةٖ مِّن فِضَّةٖ
وَأَكْوَابٖ كَانَتْ قَوَارِيراٗ ﴿15﴾ قَوَارِيراٗ مِن فِضَّةٖ قَدَّرُوهَا تَقْدِيراٗ ﴿16﴾
وَيُسْقَوْنَ فِيهَا كَأْساٗ كَانَ مِزَاجُهَا زَنجَبِيلاً ﴿17﴾ عَيْناٗ فِيهَا تُسَمَّيٰ سَلْسَبِيلاٗ ﴿18﴾
ربع
* وَيَطُوفُ عَلَيْهِمْ وِلْدَٰنٞ مُّخَلَّدُونَ إِذَا رَأَيْتَهُمْ حَسِبْتَهُمْ لُؤْلُؤاٗ مَّنثُوراٗ ﴿19﴾
وَإِذَا رَأَيْتَ ثَمَّ رَأَيْتَ نَعِيماٗ وَمُلْكاٗ كَبِيراً ﴿20﴾ عَٰلِيهِمْ ثِيَابُ سُندُسٍ
خُضْرٌ وَإِسْتَبْرَقٌ وَحُلُّواْ أَسَاوِرَ مِن فِضَّةٖ وَسَقَيٰهُمْ رَبُّهُمْ شَرَاباٗ طَهُوراً ﴿21﴾
إِنَّ هَٰذَا كَانَ لَكُمْ جَزَآءٗ وَكَانَ سَعْيُكُم مَّشْكُوراً ﴿22﴾ إِنَّا نَحْنُ
نَزَّلْنَا عَلَيْكَ اَ۬لْقُرْءَانَ تَنزِيلاٗ ﴿23﴾ فَاصْبِرْ لِحُكْمِ رَبِّكَ وَلَا تُطِعْ
مِنْهُمُۥٓ ءَاثِماً أَوْ كَفُوراٗ ﴿24﴾ وَاذْكُرِ اِسْمَ رَبِّكَ بُكْرَةٗ وَأَصِيلاٗ ﴿25﴾

6. Idaniyace mai ƙanshi bayin Allah suke sha daga gareta, suna kaita inda suka ga dama daga gidaddajinsu, sai mutum yayi tafiya a gidaddajin aljanna ga sanda a hannunsa yana nunawa ruwan inda duk yake so yaje ko yayi sama ko yayi ƙasa to saiya aikata.)
7. Suna cikawa da alwashi a cikin ɗa'ar Allah, (anan ne Sufaye suka samo dalili a kan wajabcin WURUDAN SHAIHUNNAN DARIKU in mutum ya karɓesu. Saboda nazari ana yinsa ne bisa dukkan ibadu wacce ba dolece ba,don haka in anyi nazari da salla ko azumi na farilla ko amri da ma'arufi to ya zama wajibi, haka Shehu Mukhtaru Kunti ya faɗa.) Suna tsoron rana wacce sharrinta yake madaidaici.
8. Suna ciyar da abinci ga faƙiri da maraya marar ubada ribatacce ta hanyar gaskiya, tareda son . abincin da sha'awarsa a garesu.
9. Mu muna ciyar dakune saboda neman sakamakon Allah kawai. (wato neman yardarsa,) Bama nufin sakamako daga gareku wala godiya. (wato Allah yasan wannan kyakkyawar niya da sukayi saboda haka yayi musu kirari da haka.)
10. Mu muna tsoron rana mai murtuke fuska daga Ubangijinmu. mai tsanani (a cikin murtukewar.)
11. Sai Allah ya kiyashesu sharrin wancanenka rana, ya sadasu da kyan fuska da murna.
12. Ya saka musu aljanna da tufafin alharini saboda haƙurinsu (ga buran saɓon Ubangiji).
13. Halin kasancewarsu masu kishingiɗa ne a kan gadaje na mulki, basa ganin rana a cikinsa wala hunturun sanyi (don saboda ba rana ba wata a aljanna, sai hasken Al'arshi, wanda yafi ƙarfin hasken rana.)
14. Halin kasancewarsu inuwarsu tana kusa a kansu an hore abin dasata horewa, (na kwance dana zaune da tsaye su tsinka.)
15. Ana kewayo da gidauniyoyi a cikinta da finjalai waɗanda basu da maɗauki, data kasance kaskon ƙarau.
16. Kaskon ƙarau ɗin na azurtasu masu yawone dasu, suna gwargwadasu gwargwadawa, (daidai da mashaya ba ƙari ba ragi. Malam yace "anan muka fahintacewa ko a aljanna ba almubazzaranci, inda babu abinda babu.)"
17. Ana sha dasu gidauniya a cikinta, wadda abin tsarminta ya kasance zanjabilu, (wato cittar aho.)
18. (wacce a lahira) idaniyace ake ambatonta Salsabilu, (kamar Zanjabilu wanda Larabawa suke jin daɗinsa, mai sauƙin kwarara cikin maƙogwaro.)
19. Mata suna kewayo a garesu, masu fuska sumul ba gashi, idan ka gansu zaka zace su lu'ulu'une abin daidaitawa (saboda kyansu da watsuwarsu a cikin hidima.)
20. In za kayi duba a cikinta kaga ƙasaitacciyar ni'ima da mulki mai girma ƙasaitacce.
21. Tufafin Sundusu (wato Alhariri) yana burbushinsu (wato suna saye dashi) kwarra da kakkauran dibaje, (to shi Shine na daga ciki, Sundusu kuma na daga waje,) anyi masa ado na ƙwandagai na azurfa, Ubangijinsu ya shayar dasu abin sha mai matuƙar tsarkakewa (saɓanin giyar duniya.)
22. Haƙiƙa wannan ni'ima ya kasance sakamako a gareku, aikinku ya kasance abin godewa (abin karɓa abin yarda dashi.)

(FUSKANCE-FUSKANCE GA MA'AIKIN ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAMA)

23. Haƙiƙa mu mun sassaukar da alƙur'ani a gareka sassaukarwa da ɗai ɗai (bamu saukar dashi jumla ɗaya ba.)
24. Ka haƙura da hukuncin Ubangiji gareka da iyar da aikensa, kada kabi mai zunubi dagasu kafirai ko mai yawan kafirci (Utbatu ɗan Rabi'atada Walidu ɗan Mugira da sukace ga manzan Allah Sallallahu alaihi wasallama "Komo ga buran wannan al'amarin').
25. Ka ambaci sunan ubangijinka a cikin salla, (ma'ana ka dauwama cikin salla,) asuba dayammaci (azahar da la'asar.)

وَمِنَ اَ۬ليْلِ فَاسْجُدْ لَهُۥ وَسَبِّحْهُ لَيْلاً طَوِيلاًۖ 26 إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ يُحِبُّونَ اَ۬لْعَاجِلَةَ
وَيَذَرُونَ وَرَآءَهُمْ يَوْماً ثَقِيلاًۖ 27 نَّحْنُ خَلَقْنَٰهُمْ وَشَدَدْنَآ أَسْرَهُمْ وَإِذَا شِئْنَا
بَدَّلْنَآ أَمْثَٰلَهُمْ تَبْدِيلاًۖ 28 إِنَّ هَٰذِهِۦ تَذْكِرَةٌۖ فَمَن شَآءَ اَ۪تَّخَذَ إِلَيٰ رَبِّهِۦ سَبِيلاًۖ 29
وَمَا تَشَآءُونَ إِلَّآ أَنْ يَّشَآءَ اَ۬للَّهُۖ إِنَّ اَ۬للَّهَ كَانَ عَلِيماً حَكِيماًۖ 30
يُدْخِلُ مَنْ يَّشَآءُ فِي رَحْمَتِهِۦۖ وَالظَّٰلِمِينَ أَعَدَّ لَهُمْ عَذَاباً أَلِيماًۖ 31

سُورَةُ المُرْسَلَٰتِ مَكِّيَّةٌ 77
وَهِيَ خَمْسُونَ ءَايَةً 50

بِسْمِ اِ۬للَّهِ اِ۬لرَّحْمَٰنِ اِ۬لرَّحِيمِ

وَالْمُرْسَلَٰتِ عُرْفاً 1 فَالْعَٰصِفَٰتِ عَصْفاً 2 وَالنَّٰشِرَٰتِ نَشْراً 3
فَالْفَٰرِقَٰتِ فَرْقاً 4 فَالْمُلْقِيَٰتِ ذِكْراً 5 عُذْراً اَوْ نُذْراً 6
إِنَّمَا تُوعَدُونَ لَوَٰقِعٌۖ 7 فَإِذَا اَ۬لنُّجُومُ طُمِسَتْ 8 وَإِذَا اَ۬لسَّمَآءُ فُرِجَتْ 9
وَإِذَا اَ۬لْجِبَالُ نُسِفَتْ 10 وَإِذَا اَ۬لرُّسُلُ أُقِّتَتْ 11 لِأَيِّ يَوْمٍ اُجِّلَتْ 12 لِيَوْمِ
اِ۬لْفَصْلِۖ 13 وَمَآ أَدْرَيٰكَ مَا يَوْمُ اُ۬لْفَصْلِۖ 14 وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَۖ 15
* أَلَمْ نُهْلِكِ اِ۬لْأَوَّلِينَۖ 16 ثُمَّ نُتْبِعُهُمُ اُ۬لْءَاخِرِينَۖ 17 ثمن
كَذَٰلِكَ نَفْعَلُ بِالْمُجْرِمِينَۖ 18 وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَۖ 19

26. Kuma da dare, kayi sujada gareshi (yana nufin magriba da lisha,) kayi sallar tadauwu'a dare mai tsawo (wato sulusaini ko nusfi ko sulusi.)
27. Haƙiƙa waɗannan suna son magaggauciya (duniya) suna barin rana mai nauyi bayansu (ranar alƙiyama basa aiki saboda shi.)
28 MUne muka halicccsu, muka ƙarfafa gaɓubɓansu, in imunga dama, saimu canja irinsu canjawa (maimakonsu, wato mu halakar daSU.)
29. Haƙiƙa wannan sura gargaɗice ga talikai. to wanda yaga dama saiya riƙi hanya izuwa yardar Ubungijinsa.
30. Bazaku so riƙon hanyar ɗa'a ba sai Allah ya huwace muku wannan. haƙiƙa Allah ya tabbata masani (da halittarsa,) gwani (cikin aikinsa.)
31. Yana shigar da wanda yaga dama rahamarsa (aljannarsa sune muminai,) ya tanadar wa azzalumai azaba mai raɗaɗi (sune kafirai.)

Wannan Sura Itace Sufatul Mursalati

A Makka aka saukar da ita ayoyinta hamsin ce (50)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan sura tayi zance a kan Alƙiyama da bayanin Maƙaddamomin Tashi da Ambaton Ba'alin Mabaiyanar Ikon Allah a cikin Halittaisa, sannan ambaton Halin Kafirai Ranar Alƙiyama da Halin Muminai. Ta Cika da Zargin Kafirai a bisa Ba'alin Ayyukansu.

1. ubangiji yayi rantsuwa da iskoki ababan saukowa a jere kamar gashin wuyan doki.
2. Ya rantse da iskoki ma.su tsanani.
3. Ya rantse da iskoki masu daidaita ruwa daidaitawa.
4. Ya rantse da ayoyin alƙur'ani masu rarraba tsakanin ƙarya da gaskiya rarrabewa.
5. Sannan Mala'iku masu saukar da wahayi izuwa Annabawa da Annabawa masu miƙa wahayi izuwa al'umma.
6. Don yankan hanzari ko don gargaɗi daga Allah.
7. Dahir abin nan da ake muku alwashi dashi na tashin Alƙiyama lallai mai afkuwa ne.
8. Zamanin da aka shafe hasken taurari.
9. Kuma idan sama aka keceta.
10. Idan duwarwatsu aka sheƙeta.
11. Idan manzanni aka tattarsu.
12. Ga waccc ranane mai girma akai mata iyaka?
13. (Don shaida a kan al'ummominsu da iyarwa,) saboda ranar rabe hukunci a kan halitta. (Jawabin iza, a rannan rabe hukunci tsakanin halitta ya afku.)
14. Menene yasanar dakai ranar rabewar nan (don tsoratarwa ne ga sha'aninsa.)
15. Azaba a wannan rana ta tabbata ga masu ƙaryatawa. (Wannan narko ne babba garesu.)
16. Shin bamu halakar da mutanen farko bane'? (Saboda ƙaryatawarsu. mun halakar dasu
17. Sannan mun biyar musu dana ƙarshe (daga waɗanda suka ƙaryata. kamar kafiran Makka. muka halakar dasu.)
18. Kamar yadda muka halakar da masu ƙaryatawa. haka muke aikatawa ga ma'abota laifi.
19. Azaba a ranar nan ta tabbata ga masu ƙaryatawa.

أَلَمْ نَخْلُقكُّم مِّن مَّآءٍ مَّهِينٍ ﴿20﴾ فَجَعَلْنَٰهُ فِي قَرَارٍ مَّكِينٍ ﴿21﴾ إِلَىٰ قَدَرٍ
مَّعْلُومٍ ﴿22﴾ فَقَدَّرْنَا فَنِعْمَ الْقَٰدِرُونَ ﴿23﴾ وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿24﴾
أَلَمْ نَجْعَلِ الْأَرْضَ كِفَاتًا ﴿25﴾ أَحْيَآءً وَأَمْوَٰتًا ﴿26﴾ وَجَعَلْنَا فِيهَا رَوَٰسِيَ
شَٰمِخَٰتٍ وَأَسْقَيْنَٰكُم مَّآءً فُرَاتًا ﴿27﴾ وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿28﴾
انطَلِقُوٓا إِلَىٰ مَا كُنتُم بِهِۦ تُكَذِّبُونَ ﴿29﴾ انطَلِقُوٓا إِلَىٰ ظِلٍّ ذِي ثَلَٰثِ
شُعَبٍ ﴿30﴾ لَّا ظَلِيلٍ وَلَا يُغْنِي مِنَ اللَّهَبِ ﴿31﴾ إِنَّهَا تَرْمِي بِشَرَرٍ
كَالْقَصْرِ ﴿32﴾ كَأَنَّهُۥ جِمَٰلَتٌ صُفْرٌ ﴿33﴾ وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿34﴾
هَٰذَا يَوْمُ لَا يَنطِقُونَ ﴿35﴾ وَلَا يُؤْذَنُ لَهُمْ فَيَعْتَذِرُونَ ﴿36﴾
وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿37﴾ هَٰذَا يَوْمُ الْفَصْلِ جَمَعْنَٰكُمْ وَالْأَوَّلِينَ ﴿38﴾
فَإِن كَانَ لَكُمْ كَيْدٌ فَكِيدُونِ ﴿39﴾ وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿40﴾
إِنَّ الْمُتَّقِينَ فِي ظِلَٰلٍ وَعُيُونٍ ﴿41﴾ وَفَوَٰكِهَ مِمَّا يَشْتَهُونَ ﴿42﴾ كُلُوا
وَاشْرَبُوا هَنِيٓـًٔا بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿43﴾ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجْزِي الْمُحْسِنِينَ ﴿44﴾
وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿45﴾ كُلُوا وَتَمَتَّعُوا قَلِيلًا إِنَّكُم مُّجْرِمُونَ ﴿46﴾
وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿47﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ ارْكَعُوا لَا يَرْكَعُونَ ﴿48﴾
وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿49﴾ فَبِأَيِّ حَدِيثٍ بَعْدَهُۥ يُؤْمِنُونَ ﴿50﴾

20. Shin bamu halicceku daga ruwa wulaƙantacce bane? (Shine maniyi.)
21. Muka sanyashi a mazauni amintacce (Shine mahaifa.)
22. Izuwa lokacı a bin sani lokacin haihuwa.
23. Muka hukunta wannan, Madalla masu Iko!
24. Azaba a ranar nan ta tabbata ga masu ƙaryatawa.
25. Shin bamu sanya ƙasa mai tarawa bace?
26. Rayayyu (a bayanta) da matattu (a cikinta.)
27. Muka sanya duwarwatsu maɗaukaka a cikinta. Muka shayar daku ,ruwa mai daɗi.
28. Azaba a ranar nan ta tabbata ga masu ƙaryatawa, (za ace da masu ƙaryatawa ranar Alƙiyama.)
29. "Ku tafi izuwa abinda kuka kasance kuna ƙaryatawa dashi (na azaba.)
30. "Ku tafi izuwa inuwa ma'abociyar reshe uku, (Shine hayaƙin jahannama, ın ya taso saiya kasu uku, saboda girmansa.)
31. Bamai inuwancewa ba (dazai musu maganin zafin rana,) baya wadatarwa ga buran harshen wuta.
32. Haƙiƙa ita wuta tana jitada tartsatsi kamar katanga.
33. Kai kace shi raƙuma ne baƙaƙe, (a cikin Hadisin Annabi Sallallahu alaihi wasallama yace tartsatsin wuta baƙine kamar ?mangelo.)
34. Azaba a ranar nan ta tabbata ga masu ƙaryatawa.
35. Wannan (ranar ta Alƙiyama) ranace da basa furuci da komai cikinsa.
36. Baza ayi musu izini (a cikin hanzari) ba bare suyi hanzari.
37. Azaba a ranar nan ta tabbata ga masu ƙaryatawa.
38. Wannan ranar rabe hukuncine, mun taraku (ku masu ƙaryatawa na wannan al'umma) dana mutanen farko (masu ƙaryatawa gabanku za ayi muku hisabi ayi muku azaba baki ɗaya.)
39. To in dabara ta kasance gareku a cikin ije azaba ga buranku, to kuyi mini dabarar.
40. Azaba a ranar nan ta tabbata ga masu ƙaryatawa.
41. Haƙiƙa masu jin tsoron Allah suna cikin inuwowi (na bishiyoyi, don babu rana daza tayi inuwa saboda zafinta) da marmaro (na ruwa.)
42. Da kayan marmari daga abinda suke sha'awa (Allah yasanar mana cewa abincin aljanna, gwargwadon sha'awar 'yan aljannane, saɓanin na duniya, wanda sai abinda mutane suka samu a galibi).
43. (Anace dasu) "Kuci ku sha kuna ababan yiwa barka da abinda kuka kasance kuna aikatawa.
44. Haƙiƙa yadda muka sakawa masu tsoron Allah, to hakama muke sakawa masu kyautata aiki.
45. Azaba a ranar nan tana ga masu ƙaryatawa.
46. Kuci kuji daɗi ku kafirai lokaci kaɗan (wannan ban tsoro ne garesu). haƙiƙa ku masu laifine ku.
47. Azaba a ranar nan tana ga masu ƙaryatawa.
48. In Ance dasu "Kuyi salla basa yin salla."
49. Azaba a ranar nan tana ga masu ƙaryatawa.
50. To da wane zancene bayan alƙur'ani suka bada gaskiya? (Ai bazai yiwusu ba (da gaskiya da waninsa ba, na daga littattafan Allah, bayan sun ƙaryata dashi. Saboda Alƙur'ani ya gasgata dukkan littattafan Allah. mai dacewa a asalan addini, saboda haka wanda ya ƙaryatashi, ya ƙaryata dukkan littattafan. A cikin Hadisi cewa akwai mu'ujizozin manzan Allah Sallallahu alaihi wasallama 10.070 (Dubu goma da saba'in) a cikin Alƙur'ani akwai 100.070 (Dubu ɗari da saba'in.)

حزب

78 سُورَةُ النَّبَإِ مَكِّيَّة

وَهِيَ أَرْبَعُونَ ءَايَةً 40

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

* عَمَّ يَتَسَآءَلُونَ (1) عَنِ النَّبَإِ الْعَظِيمِ (2) الَّذِے هُمْ فِيهِ مُخْتَلِفُونَ (3)
كَلَّا سَيَعْلَمُونَ (4) ثُمَّ كَلَّا سَيَعْلَمُونَ (5) أَلَمْ نَجْعَلِ الْأَرْضَ
مِهَٰداً (6) وَالْجِبَالَ أَوْتَاداً (7) وَخَلَقْنَٰكُمْ أَزْوَاجاً (8) وَجَعَلْنَا
نَوْمَكُمْ سُبَاتاً (9) وَجَعَلْنَا الَّيْلَ لِبَاساً (10) وَجَعَلْنَا النَّهَارَ مَعَاشاً (11)
وَبَنَيْنَا فَوْقَكُمْ سَبْعاً شِدَاداً (12) وَجَعَلْنَا سِرَاجاً وَهَّاجاً (13) وَأَنزَلْنَا
مِنَ الْمُعْصِرَٰتِ مَآءً ثَجَّاجاً (14) لِّنُخْرِجَ بِهِۦ حَبّاً وَنَبَاتاً (15) وَجَنَّٰتٍ أَلْفَافاً (16)
إِنَّ يَوْمَ الْفَصْلِ كَانَ مِيقَٰتاً (17) يَوْمَ يُنفَخُ فِي الصُّورِ فَتَأْتُونَ أَفْوَاجاً (18)
وَفُتِّحَتِ السَّمَآءُ فَكَانَتْ أَبْوَٰباً (19) وَسُيِّرَتِ الْجِبَالُ فَكَانَتْ سَرَاباً (20)
إِنَّ جَهَنَّمَ كَانَتْ مِرْصَاداً (21) لِّلطَّٰغِينَ مَـَٔاباً (22) لَّبِثِينَ فِيهَا أَحْقَاباً (23)
لَّا يَذُوقُونَ فِيهَا بَرْداً وَلَا شَرَاباً (24) إِلَّا حَمِيماً وَغَسَّاقاً (25) جَزَآءً وِفَاقاً (26)
إِنَّهُمْ كَانُوا لَا يَرْجُونَ حِسَاباً (27) وَكَذَّبُوا بِـَٔايَٰتِنَا كِذَّاباً (28) وَكُلَّ
شَےْءٍ أَحْصَيْنَٰهُ كِتَٰباً (29) فَذُوقُوا فَلَن نَّزِيدَكُمْ إِلَّا عَذَاباً (30)

Wannan Sura Itace Suratul Naba'i
A Makka aka saukar •da ita aya arba'incc (40)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan Sura tayi zance a kan Tashi da Bayanin Mabaiyanar Ikon Allah da Magana kan Musun Tashin Alƙiyama).

1. Da wane abune ƙuraishu ba'alinsu ke tambayon ba'ali?
2. Ga babbar magana ne.
3. Wanda suke saɓawa cikinsa, Muminai suke gaskatawa, kafirai suke ƙaryatawa, Shine abinda Annabi yazo dashi na Alƙur'ani wanda ya tattarar bisa tashin Alƙiyama da waninsa.
4. Tsawa, da sannu zasu san (abinda zai samu garesu bisa inkarin da sukeyi.)
5. Sannan Ahir! da sannu zasu san abinda zai sauka garesu saboda musunsu gashi.
6. Shin bamu .sanya ƙasa, kamar gunya ga yaro wato shinfiɗar yaro jariri ba?
7. Bamu halicci duwatsu turaku ga ƙasa ba, (da ƙasa take tabbata dasu?)
8. Mun haliccc ku mazaje da mataye.
9. .Mun sanya baccinku hutu ga jikkunanku.
10. Mun sanya dare tufafi mai suturcewa da baƙinsa.
11. Mun sanya wuni lokacin cin abinci.
12. Mun gina sammai bakwai ƙarfafa birbishinku (wanda yau da kullum bazai musu tasirin komai ba.)
13. Mun sanya fitila mai yawan huruwa (wato rana).
14. Mun saukar da ruwa daga gizagizai waɗanda suke sintsirarru da ruwa.

(ALMU'USIRU A LUGGA YARINYAR DATA ISA HAIHUWA)

15. Donmu fitar da ƙwaya dashi (kamar alkama,) da tsiri (kamar) ƙaiayi.)
16. Mun sanya gonakai masararraka da itatuwa.
17. Haƙiƙa ranar rabe hukunci tsakanin talikai ya kasance lokacin sakamako da uƙuba a gareku.
18. Ranar da ake busa cikin ƙaho. Mala'ika Israfilu Shine mai busar, kuzo daga kaburburanku, bundu-bundu, (wato jama'a dabam-daban.)

(ƘARYATAWAR MASU CEWA SAMA FILICE KAWAI)

19. Za a kece sammai saboda saukar Mala'iku.
20. Za a tafiyar da duwarwatsai ga buran gurarenta ta zama ƙurar taga abar sheƙewa.
21. Haƙiƙa jahannama ta kasance madakata.
22. Ga kafirai masu shishshigi, makomace (a garesu.)
23. Ababan zama a cikinta zamanai na badada (wato lokaci ba iyaka.)
24. BazaSU ɗanɗani bacci ba a cikinta wala abin sha na jin daɗi.
25. Saidai ruwa tafashashshe da ruwan miƙki mai kwarara.
26. Sakamako mai dacewa (da aikinsu domin ba zunubi mafi girma daga kafirci, ba azaba mafi girma daga wuta.)
27. Haƙiƙa su sun kasance basa tsoron sakamako, Don sunyi musun tashi.
28. Sun ƙaryata da ayoyinmu (alƙur'ani) ƙaryatawa.
29. Mun ƙirge kowane abu na daga aiyuka a rubuce (a Lauhil Mahfuzu, don muyi sakaiya a kansa, ƙaryatawar Alƙur'ani yana daga wancancnka ana cewa daSU ranar alƙiyama.)
30. "KU ɗanɗani sakamakonku bazamu daɗa muku komai ba sai azabarku burbushinku."

إِنَّ لِلْمُتَّقِينَ مَفَازًا ﴿31﴾ حَدَآئِقَ وَأَعْنَابًا ﴿32﴾ وَكَوَاعِبَ أَتْرَابًا ﴿33﴾ وَكَأْسًا
دِهَاقًا ﴿34﴾ لَّا يَسْمَعُونَ فِيهَا لَغْوًا وَلَا كِذَّٰبًا ﴿35﴾ جَزَآءً مِّن رَّبِّكَ عَطَآءً
حِسَابًا ﴿36﴾ رَّبِّ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا الرَّحْمَٰنِ لَا يَمْلِكُونَ
مِنْهُ خِطَابًا ﴿37﴾ يَوْمَ يَقُومُ الرُّوحُ وَالْمَلَٰٓئِكَةُ صَفًّا لَّا يَتَكَلَّمُونَ
إِلَّا مَنْ أَذِنَ لَهُ الرَّحْمَٰنُ وَقَالَ صَوَابًا ﴿38﴾ ذَٰلِكَ الْيَوْمُ الْحَقُّ فَمَن شَآءَ
اتَّخَذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ مَـَٔابًا ﴿39﴾ إِنَّآ أَنذَرْنَٰكُمْ عَذَابًا قَرِيبًا يَوْمَ يَنظُرُ
الْمَرْءُ مَا قَدَّمَتْ يَدَاهُ وَيَقُولُ الْكَافِرُ يَٰلَيْتَنِي كُنتُ تُرَٰبًا ﴿40﴾

سُورَةُ النَّازِعَاتِ مَكِّيَّةٌ 79

وَهِيَ خَمْسٌ وَأَرْبَعُونَ ءَايَةً 45

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

ثمن

* وَالنَّٰزِعَٰتِ غَرْقًا ﴿1﴾ وَالنَّٰشِطَٰتِ نَشْطًا ﴿2﴾ وَالسَّٰبِحَٰتِ سَبْحًا ﴿3﴾
فَالسَّٰبِقَٰتِ سَبْقًا ﴿4﴾ فَالْمُدَبِّرَٰتِ أَمْرًا ﴿5﴾ يَوْمَ تَرْجُفُ الرَّاجِفَةُ ﴿6﴾
تَتْبَعُهَا الرَّادِفَةُ ﴿7﴾ قُلُوبٌ يَوْمَئِذٍ وَاجِفَةٌ ﴿8﴾ أَبْصَٰرُهَا خَٰشِعَةٌ ﴿9﴾ يَقُولُونَ
أَءِنَّا لَمَرْدُودُونَ فِي الْحَافِرَةِ ﴿10﴾ أَءِذَا كُنَّا عِظَٰمًا نَّخِرَةً ﴿11﴾ قَالُوا تِلْكَ إِذًا كَرَّةٌ
خَاسِرَةٌ ﴿12﴾ فَإِنَّمَا هِيَ زَجْرَةٌ وَاحِدَةٌ ﴿13﴾ فَإِذَا هُم بِالسَّاهِرَةِ ﴿14﴾

31. Masu (tsoron Allah suna da matsera a aljanna.
32. Rafika da inabai.
33. Da 'yan mata wađanda nononsu yake a tsaitsaye, a bisa tsareku, (wato masu shekara đaya).
34. Da gidauniya ta giya mai cika finjalanta.
35. Basa jin zancen banza (a cikin aljanna yayin shan giya na daga haluluwa,) wala ƙaryatawar juna, (sabanin abinda yake afkuwa a duniya, yayin shan giya.)
36. Don sakamako daga Ubangijinka, kyauta mai yawa, mai isuwa, (komai wadatarwa.)
37. Ubangijin sammai da ƙassai da abinda yake tsakaninsu, Sarki mai ishashshiyar rahama, su talikai basu mallaki zance daga gun Ubangiji ba, (wato ba mai iya magana dashi daga cikinsu don tsoronsa).

(CETON MUMINAI DA MALA'IKU)

38. Ranar da Mala'iku da Mala'ika Jibrilu suke tsayawa sahu-sahu, talikai basu da ikon yin zance, sai wanda Ubangiji mai tsananin jinƙai yayi izini gareshi a cikin yin zance, yayi magana ta taƙaitarta. (sune Muminai da Mala'iku, ya basu izini ga wanda yayi musu izini su ceceshi. Malam yace: Allah ya tabbata Muminai suna ceto a ranar Lahira. 'yan bidi'a wato Wahabiyyawa suna musunsa. sunyi karo da tabbataccen Nassi na Alƙur'ani, Allah ya kiyashemu.)
39. Wancanenka Shine rana ta gaskiya (wadda lallai saita afku, Itace Alƙiyama,) wanda yaga dama zai riƙi komawa izuwa Ubangijinsa (da biyayya gareshi don yakuɓuta daga azaba.)
40. Haƙiƙa mu mun firgitar daku ,(ya kafiran Makka) azaba makusanciya, ranar Alƙiyama mai zuwace, dukkan mai zuwa makusancine, ranar da mutum zai duba abinda hannuwansa ta gabbatar na hairi ko sharri, kafiri zaice wayyo Allah, dayakace ni na zama turɓaya, (baza ayi min azaba ba, zai fađi wannan yayin da Allah zaice da dabbobi, bayan an yi ƙisasi, shashinta daga sashi, "ku zamo turɓaya.")

Wannan Sura Itace Suratu Nazi'ati

A Makka aka saukar da ita aya arba'in da biyarce (45)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba đaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan Sura tayi zance a kan Rantsuwa da Taurari da Mala'iku a bisa Tashi, da baiwa Mushurkai tsoro da ambaton ƙissar Fir'auna da ƙarshensa da ba'alin mabaiyanar Ikon Allah, dacewar Halittar mutane yafi ƙaranci daga waninsa da bayanin halinsu ranar Alƙiyama, an cika da ba'alin haƙƙoƙi da suka ' rataya da ranar Tashi.)

1. Ubangiji ya rantse da Mala'iku masu fizgar rayukan kafirai. fizga mai tsanani.
2. Da masu zare rayukan mummai zara mai sauƙi.
3. Da masu ninkaya da Limamin Ubangiji daga sama ninkaya.
4. Da Mala'iku masu tsere da rayukan Muminai izuwa Aljanna tsere.
5. Da Mala'iku masu saukarwar shirye-shiryen rayuwar duniya na halitta (na al'amarin duniya, Wallahi za a tasheku ya kafiran Makka.)
6. Ranar da magirgijiya take girgiza (a busar farko).
7. Mai kuturna take binta. (Mai kuturna Itace busa ta biyu tsakaninsu shekara 40).
8. Zukata a wannan rana suna makyarkyata.
9. Gannanta suna tursashe.
10. (Ma abota hankula da basira suna fađa don izgili da musun tashi.) "Shin yanzu za a maida mu izuwa rayuwa idan mun mutu?"
11. Ashe (masake rayuwa) in mun zama ƙasusuwa rididdigaggu?
12. Sukace "wancananka (wato komawarmu izuwa rayuwa in ta inganta) komowace taɓaɓɓiya."
13. Ubangiji yace, "dahir ita makuturniya busace guda đaya".
14. Idan aka busata saiga talikai dukkansu a fuskar ƙasa (wacce ake kiranta Sahiratu watau mai tarmazazai an ambace ta haka saboda ban tsoro gareta da baƙin ciki.

هَلْ أَتَاكَ حَدِيثُ مُوسَىٰ ﴿15﴾ إِذْ نَادَاهُ رَبُّهُ بِالْوَادِ الْمُقَدَّسِ طُوًى ﴿16﴾
اذْهَبْ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ إِنَّهُ طَغَىٰ ﴿17﴾ فَقُلْ هَل لَّكَ إِلَىٰ أَن تَزَكَّىٰ ﴿18﴾ وَأَهْدِيَكَ
إِلَىٰ رَبِّكَ فَتَخْشَىٰ ﴿19﴾ فَأَرَاهُ الْآيَةَ الْكُبْرَىٰ ﴿20﴾ فَكَذَّبَ وَعَصَىٰ ﴿21﴾ ثُمَّ
أَدْبَرَ يَسْعَىٰ ﴿22﴾ فَحَشَرَ فَنَادَىٰ ﴿23﴾ فَقَالَ أَنَا رَبُّكُمُ الْأَعْلَىٰ ﴿24﴾ فَأَخَذَهُ
اللَّهُ نَكَالَ الْآخِرَةِ وَالْأُولَىٰ ﴿25﴾ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَعِبْرَةً لِّمَن يَخْشَىٰ ﴿26﴾
أَأَنتُمْ أَشَدُّ خَلْقًا أَمِ السَّمَاءُ بَنَاهَا ﴿27﴾ رَفَعَ سَمْكَهَا فَسَوَّاهَا ﴿28﴾
وَأَغْطَشَ لَيْلَهَا وَأَخْرَجَ ضُحَاهَا ﴿29﴾ وَالْأَرْضَ بَعْدَ ذَٰلِكَ دَحَاهَا ﴿30﴾ أَخْرَجَ
مِنْهَا مَاءَهَا وَمَرْعَاهَا ﴿31﴾ وَالْجِبَالَ أَرْسَاهَا ﴿32﴾ مَتَاعًا لَّكُمْ وَلِأَنْعَامِكُمْ ﴿33﴾
فَإِذَا جَاءَتِ الطَّامَّةُ الْكُبْرَىٰ ﴿34﴾ يَوْمَ يَتَذَكَّرُ الْإِنسَانُ مَا سَعَىٰ ﴿35﴾
وَبُرِّزَتِ الْجَحِيمُ لِمَن يَرَىٰ ﴿36﴾ فَأَمَّا مَن طَغَىٰ ﴿37﴾ وَآثَرَ الْحَيَاةَ
الدُّنْيَا فَإِنَّ الْجَحِيمَ هِيَ الْمَأْوَىٰ ﴿38﴾ وَأَمَّا مَنْ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِ
وَنَهَى النَّفْسَ عَنِ الْهَوَىٰ ﴿39﴾ فَإِنَّ الْجَنَّةَ هِيَ الْمَأْوَىٰ ﴿40﴾
۞ يَسْأَلُونَكَ عَنِ السَّاعَةِ أَيَّانَ مُرْسَاهَا ﴿41﴾ فِيمَ أَنتَ مِن ذِكْرَاهَا ﴿42﴾
إِلَىٰ رَبِّكَ مُنتَهَاهَا ﴿43﴾ إِنَّمَا أَنتَ مُنذِرُ مَن يَخْشَاهَا ﴿44﴾
كَأَنَّهُمْ يَوْمَ يَرَوْنَهَا لَمْ يَلْبَثُوا إِلَّا عَشِيَّةً أَوْ ضُحَاهَا ﴿45﴾

ربع

15. Hak̃ik̃a labarin Annabi Musa yazo maka.
16. Zamanin da Ubangijinsa ya kirashi a Wadi (zaza) abin tsarkakewa wanda sunansa Đuwa.
17. Tafi izuwa Fir'auna hak̃ik̃a shi yayi shishshigi, (ya k̃etara haddi.)
(YADDA AKE KIRA IZUWA UBANGIJI DA TAUSHI BADA HAYAGAGA KO ZAGE- ZAGE BA)
18. Kace "kana da buk̃ata izuwa ka tsarkaka?
19. "In shiryeka izuwa Ubangijinka,sai kaji tsoro".
20. Saiya nuna masa babbar aya.
21. Sai yak̃aryata.
22. Saiya gırka da baya yana mai ɓarna a bayan k̃asa.
23. Ya tara (matsafa da rundunarsa) ya kirawo rundunar).
24. Yace nine Ubangijinku mafi girma.
25. Sai Ubangiji ya dank̃eshi (da nutsarwa, Ubangiji ya dank̃eshi) uk̃ubar wannan kalma data farko (wacce Itace faɗinsa "bansan kunada wani Allah baniba", tsakanin waccen ta farkon data biyun akwai shekara 40).
26. "(Yace)" akwai izna a cikin wancananka ga mai jin tsoron Allah.
27. ("Yace)" kune kuka fi k̃arfin halittane ko sama daya ginata?
28. "Ya dasa rufinta, ya daidaita ta,
29. "Ya duhunta darenta, ya fitar da walaharta
30. "Ya shimfiɗe k̃asa bayan wannan shinfiɗewa (ta kasance gaban halitta bada shimfiɗewa ba. dacan ta kasance gaban sama ba tareda shimfiɗewa ba.")
31. "Yafitar da ruwanta daga gagreta. (da ɓuɓɓugar da idandunanta.) da makiyayà ta abincin dabbobi da mutane."
32. "Ya tabbatar da duwarwatsu tabbatarwa do ku nutsu."
33. "Don jiyawar daɗi garekuda dabbobinku (IBLU da GANAMU da BAK̃ARU)"
34. Idan mai ɗume kunne Itace mafi girma tazo (Itace busa ta biyu.)
35. Ranar da mutum zai tuna abinda ya aikata." (na hairi ko sharri)
36. Aka baiyana wuta mai k̃onewa ga dukkan mai duba.
37. To amma wanda yayi shishshigi da kafirci yafifita duniya da abin sha'awaice-sha'awaice.
38. To hak̃ik̃a jahannama Itace makomarsa.
39. Amma wanda yaji tsoron tsaiwa gaban Ubangijinsa ya hana kansa muguwa, ammara ga buran hawa.
40. To hak̃ik̃a Aljanna Itace makomarsa (yadda dai abin yake mai saɓo yana cikin wuta, maibi yana cikin aljanna.)
41. Suna tambayon ka tashin alk̃iyama, yaushe ne aukuwata?
42. A cikin wane abu kake daga ambatonta (ma'ana baka da iliminta, bare ka ambaceta.)
43. Izuwa Ubangijine matuk̃ar saninta (banda Allah ba wanda yasan sandaza ayità).
44. Kai kawai kana gargaɗin wanda yake jin tsoronta.
45. Kai kace ranar dasuke ganinta basu zauna (a cikin kaburburansu) basai yammaci ko walaharta.

سُورَةُ عَبَسَ مَكِّيَّة 80

وَهِيَ إِحْدَىٰ وَأَرْبَعُونَ ءَايَةً 41

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

عَبَسَ وَتَوَلَّىٰٓ ﴿1﴾ أَن جَآءَهُ الْأَعْمَىٰ ﴿2﴾ وَمَا يُدْرِيكَ لَعَلَّهُۥ يَزَّكَّىٰٓ ﴿3﴾
أَوْ يَذَّكَّرُ فَتَنفَعَهُ الذِّكْرَىٰٓ ﴿4﴾ أَمَّا مَنِ اسْتَغْنَىٰ ﴿5﴾ فَأَنتَ لَهُۥ
تَصَدَّىٰ ﴿6﴾ وَمَا عَلَيْكَ أَلَّا يَزَّكَّىٰ ﴿7﴾ وَأَمَّا مَن جَآءَكَ يَسْعَىٰ ﴿8﴾
وَهْوَ يَخْشَىٰ ﴿9﴾ فَأَنتَ عَنْهُ تَلَهَّىٰ ﴿10﴾ كَلَّآ إِنَّهَا تَذْكِرَةٌ ﴿11﴾ فَمَن
شَآءَ ذَكَرَهُۥ ﴿12﴾ فِي صُحُفٍ مُّكَرَّمَةٍ ﴿13﴾ مَّرْفُوعَةٍ مُّطَهَّرَةٍ ﴿14﴾
بِأَيْدِي سَفَرَةٍ ﴿15﴾ كِرَامٍ بَرَرَةٍ ﴿16﴾ قُتِلَ الْإِنسَانُ مَآ أَكْفَرَهُۥ ﴿17﴾
مِنْ أَيِّ شَيْءٍ خَلَقَهُۥ ﴿18﴾ مِن نُّطْفَةٍ خَلَقَهُۥ فَقَدَّرَهُۥ ﴿19﴾ ثُمَّ السَّبِيلَ
يَسَّرَهُۥ ﴿20﴾ ثُمَّ أَمَاتَهُۥ فَأَقْبَرَهُۥ ﴿21﴾ ثُمَّ إِذَا شَآءَ أَنشَرَهُۥ ﴿22﴾ كَلَّا
لَمَّا يَقْضِ مَآ أَمَرَهُۥ ﴿23﴾ فَلْيَنظُرِ الْإِنسَانُ إِلَىٰ طَعَامِهِۦٓ ﴿24﴾ إِنَّا صَبَبْنَا
الْمَآءَ صَبًّا ﴿25﴾ ثُمَّ شَقَقْنَا الْأَرْضَ شَقًّا ﴿26﴾ فَأَنۢبَتْنَا فِيهَا حَبًّا ﴿27﴾
وَعِنَبًا وَقَضْبًا ﴿28﴾ وَزَيْتُونًا وَنَخْلًا ﴿29﴾ وَحَدَآئِقَ غُلْبًا ﴿30﴾ وَفَٰكِهَةً
وَأَبًّا ﴿31﴾ مَّتَٰعًا لَّكُمْ وَلِأَنْعَٰمِكُمْ ﴿32﴾ * فَإِذَا جَآءَتِ الصَّآخَّةُ ﴿33﴾

ثمن

Wannan Sura Itace Suratu A'ama

A Makka aka saukar da ita aya arba'in da biyuce (42)
Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan Sura tayi zance a kan Abdullahi ibnu Ummi makhtumi, Alƙur'ani gargaɗine wanda yaga dama ya gargaɗu dashi. Tayi bayani a kan asalin mutum da faruwarsa da abincinsa da abin shansa da rayuwar Lahira da abinda yake cikinsa.)

I. Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) ya ɗaure fuskarsa ya bijire.
2. Don makaho yazo masa (Abdullahi ɗan ummi Makhtumi ya yankeshi daga abinda yake tafe dashi saboda wanda yake ƙaunar Musuluncinsa daga manyan ƙuraishu, shi wannan makaho bai san ya shagala da wannan ba saiya kirawoshi yace "sanar dani daga abinda Allah yasanar da kai." sai manzon Allah ya juya izuwa gidansa, sai akayi masa magana da abinda ya sauka, saiya zama duk sanda yazo sai Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) yace "marabada wanda Ubangijina yayi mini magana cikin sha'aninsa." saiya shimfiɗa masa mayafinsa ya zauna.
3. Me yasanar dakai cewa watakila shi zai tsarkaka (gareka daga abinda yake yi daga gareka?)
4. Koya wa'azantu gargaɗi ta amfaneshi?
5. Amma wanda ya wadata da dukiya.
6. To kai kana fuskantarsa.
7. Ba cuta a kankan in bai bada gaskiya ba.
8. Amma wanda yazo maka yana garaje.
9. Alhali shi yana tsoron Allah (Shine makahon nan).
10. To kai kana shagala ga buransa.
11. Kadaka kuma aikata irin wannan. ita wannan sura gargaɗi ce ga talikai.
12. To wanda yaga dama ya kiyaye wannan ya wa'azantu dashi.
13. A cikin littattafai ababan girmamawa gun Allah.
14. Abar ɗaukakawa (gurin Allah a cikin sama) abar tsarkakewa (ga buran shafar shaiɗanu.)
15. A hannun marubuta (dasuke rubutota daga Lauhil Mahfuzu).
16. Masu girma masu biyayya (ga Allah sune Mala'iku).
17. An tsinewa kafiri, mana ki abinda ya ɗaukeshi kan kafirai!
18. Daga wane abu ya halicceShine?
19. Daga ɗigon maniyi ya halicce shiya gwargwadashi (gudan jini sannan tsoka izuwa ƙarshen halittarsa.)
20. Sannan ya hore masa hanyar fitowa daga cikin uwarsa.
21. Sannan ya karɓi ransa, sai kuma ya shigar dashi cikin kabari.
22. Sannan in yaga dama ya raya shi don tashi.
23. Dahir kafiri bai aikata abinda Ubangijinsa ya umarce shi dashi ba.
24. Mutum yayi duba izuwa abincinsa (yayaya ƙaddara shi aka shirya masa shi?)
25. Haƙiƙa mun kwararo ruwane (daga sama) kwararowa.
26. Sannan muka keta ƙasa da tsiri ketawa.
27. Muka tsirar da ƙwaya a cikinta kamar .;alkama da sha'ir.
28. Da inabi da haniwar gaɗagi.
29. Da zaitun (wato bishiyar da ake kiranta atule Itace zaitun) da dabino.
30. Da gonakai masararraka da itatuwa.
31. Da abin marmari da makiyayar dabbobi.
32. Don jiyarwar daɗi gareku da dabbobinku.

يَوْمَ يَفِرُّ الْمَرْءُ مِنْ أَخِيهِ ﴿33﴾ وَأُمِّهِ وَأَبِيهِ ﴿34﴾ وَصَاحِبَتِهِ وَبَنِيهِ ﴿35﴾
لِكُلِّ امْرِئٍ مِّنْهُمْ يَوْمَئِذٍ شَأْنٌ يُغْنِيهِ ﴿36﴾ وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ
مُّسْفِرَةٌ ﴿37﴾ ضَاحِكَةٌ مُّسْتَبْشِرَةٌ ﴿38﴾ وَوُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ عَلَيْهَا غَبَرَةٌ ﴿39﴾
تَرْهَقُهَا قَتَرَةٌ ﴿40﴾ أُولَٰئِكَ هُمُ الْكَفَرَةُ الْفَجَرَةُ ﴿41﴾

81 سُورَةُ التَّكْوِيرِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ ثَمَانٍ وَعِشْرُونَ ءَايَةً 28

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

إِذَا الشَّمْسُ كُوِّرَتْ ﴿1﴾ وَإِذَا النُّجُومُ انكَدَرَتْ ﴿2﴾ وَإِذَا الْجِبَالُ
سُيِّرَتْ ﴿3﴾ وَإِذَا الْعِشَارُ عُطِّلَتْ ﴿4﴾ وَإِذَا الْوُحُوشُ حُشِرَتْ ﴿5﴾
وَإِذَا الْبِحَارُ سُجِّرَتْ ﴿6﴾ وَإِذَا النُّفُوسُ زُوِّجَتْ ﴿7﴾ وَإِذَا الْمَوْءُودَةُ
سُئِلَتْ ﴿8﴾ بِأَيِّ ذَنبٍ قُتِلَتْ ﴿9﴾ وَإِذَا الصُّحُفُ نُشِرَتْ ﴿10﴾
وَإِذَا السَّمَاءُ كُشِطَتْ ﴿11﴾ وَإِذَا الْجَحِيمُ سُعِّرَتْ ﴿12﴾ وَإِذَا الْجَنَّةُ
أُزْلِفَتْ ﴿13﴾ عَلِمَتْ نَفْسٌ مَّا أَحْضَرَتْ ﴿14﴾ * فَلَا أُقْسِمُ بِالْخُنَّسِ ﴿15﴾ رُبع
الْجَوَارِ الْكُنَّسِ ﴿16﴾ وَاللَّيْلِ إِذَا عَسْعَسَ ﴿17﴾ وَالصُّبْحِ إِذَا تَنَفَّسَ ﴿18﴾
إِنَّهُ لَقَوْلُ رَسُولٍ كَرِيمٍ ﴿19﴾ ذِي قُوَّةٍ عِندَ ذِي الْعَرْشِ مَكِينٍ ﴿20﴾

33. To idan mai dishe kunne tazo muku (busa ta biyu).
34. Ranar da mutum yake gujewa ɗan uwansa.
35. Da uwarsa da ubansa.
36. Da matarsa da 'ya'yansa.
37. Kowane mutum daga garesu a wannan rana yana da sha'ani dazai shagalar dashi (ga buran sha'anin waninsa, fuskoki a wannan rana kashi biyu ne.)
38. Fuskoki masu haske.
39. Masu dariya masu murna. (sune Muminai.)
40. Da fuskoki a wannan rana ƙura na kanta.
41. Duhu yana lulluɓeta.
42. Wadancanenka (ma'abota wan nan hali) sune kafirai fajirai (Allah ya kiyashemu.)

Wannan Sura Itace Suratu Takwiri

A Makka aka saukar da ita aya ishirin da tara ce (29)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan Sura ta ƙunshi magana a kan tashi da muƙaddamominsa rantsuwa a kan Alƙur'ani gaskiya ne, an. aiko dashi a bisa harshen Jibrilu izuwa Annabi Sallallahu alaihi waSallama.)

1. Idan rana aka naɗeta aka tafiyar da haskenta.
2. Idan taurari suka gurbace (suka zubo a kan ƙasa.)
3. Idan duwatsu aka tafiyar da ita (ga buran fuskar ƙasa ta zama kamar ƙurar taga abar shaƙewa.)
4. Idan raƙuma masu cikin wata goma aka barta bada mai kiwo ba, (saboda abinda ya damesu na daga lamari, ba dukiyar da tafi soyuwa garesu daga raƙu ma.)
5. Lokacin da namun daji aka tarasu (bayan tashi don ayi hisabi, ba'ali daga ba'ali.)
6. Lokacin da koguna aka ƙoneta (ta zama wuta.)
7. Lokacin da kawuka aka haɗata da jikkunanta.
8. Lokacin da yarinya da akabinneta da rai don tsoron laifi da buƙata, aka tambayeta.
9. Da wane zunubi ne aka kasheta? (Za Tace an kashe ni bada laifi ba.)
10. Lokacin da takardu aka daidaitata.
11. Lokacin da sama aka kauda ita (ga buran gurararan zamanta tamfar da ake kwaye fata ga buran akuya.)
12. Lokacin da wuta aka hurata.
13. Lokacin da Aljanna aka kusanta ta, (ga mazowanta donsu shigeta. to jawabin abubuwan da suka gabata shine).
14. Kowace rai tasan abindata aikata na hairi ko sharri.
15. Ni ina rantsuwa da taurari masu noƙewa!
16. Masu gudu (a cikin falaki. sune masu faɗuwa a guren da take faɗuwa a cikinta. sune taurari guda biyar, zuhal. mushtari. mirriha. zuhharair da udaridu) masu noƙewa. wato tana komowa a cikin fagen sukuwarta. tana komowa da baya yanzu-yanzun nan kana ganin tauraro a ƙarshen buruji sai kaga yakomo izuwa farkonsa).
17. Ina rantsuwa da dare idan yagabato (koya juya) da duhunsa.
18. Ina rantsuwa da asuba idan yayi numfashi. (wato ya miƙu har rana ta bayyana.)
19. Haƙiƙa wannan Alƙur'ani lallai maganar manzo ne mai girma (ga Allah Shine manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama.)
20. Ma'abocin ƙarfi nan ga Ubangijin Aƙarshe, matabbacin daraja.

مُطَاعٖ ثَمَّ أَمِينٖ ﴿21﴾ وَمَا صَاحِبُكُم بِمَجْنُونٖ ﴿22﴾ وَلَقَدْ رَءَاهُ بِالْأُفُقِ
الْمُبِينِ ﴿23﴾ وَمَا هُوَ عَلَى الْغَيْبِ بِضَنِينٖ ﴿24﴾ وَمَا هُوَ بِقَوْلِ شَيْطَٰنٖ رَّجِيمٖ ﴿25﴾
فَأَيْنَ تَذْهَبُونَ إِنْ هُوَ إِلَّا ذِكْرٞ لِّلْعَٰلَمِينَ ﴿26﴾ لِمَن شَآءَ مِنكُمْ
أَن يَسْتَقِيمَ ﴿27﴾ وَمَا تَشَآءُونَ إِلَّا أَن يَشَآءَ اللَّهُ رَبُّ الْعَٰلَمِينَ ﴿28﴾

82 سورة الانفطار مكية

وهي تسع عشرة ءاية 19

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

إِذَا السَّمَآءُ انفَطَرَتْ ﴿1﴾ وَإِذَا الْكَوَاكِبُ انتَثَرَتْ ﴿2﴾ وَإِذَا الْبِحَارُ
فُجِّرَتْ ﴿3﴾ وَإِذَا الْقُبُورُ بُعْثِرَتْ ﴿4﴾ عَلِمَتْ نَفْسٞ مَّا قَدَّمَتْ وَأَخَّرَتْ ﴿5﴾
يَٰأَيُّهَا الْإِنسَانُ مَا غَرَّكَ بِرَبِّكَ الْكَرِيمِ ﴿6﴾ الَّذِي خَلَقَكَ فَسَوَّيٰكَ
فَعَدَّلَكَ ﴿7﴾ فِي أَيِّ صُورَةٖ مَّا شَآءَ رَكَّبَكَ ﴿8﴾ كَلَّا بَلْ تُكَذِّبُونَ بِالدِّينِ ﴿9﴾
وَإِنَّ عَلَيْكُمْ لَحَٰفِظِينَ ﴿10﴾ كِرَامٗا كَٰتِبِينَ ﴿11﴾ يَعْلَمُونَ مَا تَفْعَلُونَ ﴿12﴾
إِنَّ الْأَبْرَارَ لَفِي نَعِيمٖ ﴿13﴾ وَإِنَّ الْفُجَّارَ لَفِي جَحِيمٖ ﴿14﴾ يَصْلَوْنَهَا يَوْمَ الدِّينِ ﴿15﴾
وَمَا هُمْ عَنْهَا بِغَآئِبِينَ ﴿16﴾ وَمَا أَدْرَيٰكَ مَا يَوْمُ الدِّينِ ﴿17﴾ ثُمَّ مَا أَدْرَيٰكَ مَا يَوْمُ
الدِّينِ ﴿18﴾ يَوْمَ لَا تَمْلِكُ نَفْسٞ لِّنَفْسٖ شَيْـٔٗا وَالْأَمْرُ يَوْمَئِذٖ لِّلَّهِ ﴿19﴾

21. Abinbi a cikin sama (Mala'iku suna binsa da Annabawa,) Amintacce kan wahayi.
22. Abokinku (Annabi Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama) bai kasance mahaukaci ba (tamfar da kuka raya.)
23. Haƙiƙa Annabi Muhammadu (Sallallahu alaihi wasallama) yaga Jibrila (Alaihisallamu a bisa surarsa wacce aka halicce shi a kansa) a sassa mabayyani (a nahiyar gabas.)
24. Shi (Annabi Sallallahu alaihi wasallama) bai kasance mai rowa ga wahayi ba.
25. Shi kuma Alƙ.ur'ani ba maganar shaiɗan abin tsinewane ba.
26. Ina kuke zuwane, (a cikin musun Alƙur'ani da bijirewarku ga buransa.)
27. Shi (Alƙur'ani) bai kasance ba sai gargaɗi ga talikai (mutane da aljanu.)
28. Ga wanda yaga dama ya daidai ta (kan gaskiya) daga cikinku.
29. Bazaku sami damar ku tsaya kan gaskiya ba, sai in Allah Ubangijin talikai yanufi (daidaituwarku a kansa.)

Wannan Sura Itace Suratul Infidari

A Makka aka saukar da ita aya goma sha tara ce (19)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan Sura tayi zance a kan Tashin Alƙiyama da gargaɗi da ranar Alƙiyama cewa kai zai ga abinda ya aikata, sannan munaƙashar mutum a cikin saɓawa Ubangijinsa tareda ni'imar Allah a gareshi yasanya masa shaidu masu rubuta aikinsa, sannan ƙarshen kowa Wuta ko Aljanna, lamari na Allah ne.)

1. Yayin da sama ta kece.
2. Yayin da taurari suka zubo.
3. Yayin da koguna aka keceta (ta zama kogi ɗaya na daɗi ya cuɗanya dana zartsi.)
4. Yayin da kaburbura aka toneta, (jawabi...)
5. Kowace kai tasan abindata aikata (a wannan rana) da abinda ta jinkirtar (nasa da wanda bata aikatashi ba.)
6. Ya wannan mutum kafirai, meya ruɗeka da Ubangijinka mai karamci (harka saɓeshi.)
7. Wanda ya halicceka (bayan baka,) ya daidaita halittarka (yasanya ka madaidaicin halitta lafiya sumul, madaidaicin gaba.)
8. A cikin kowace irin surace ya ɗoraka ya rakkabaka.
9. Bari ruɗuwa da Karamcin Allah! bari! ku kafiran Makka kuna ƙaryatawa da sakamakon ayyuka.
10. Haƙiƙa akwai masu kiyayewar ayyuka na Mala'iku.
11. Masu girma (gun Allah,) masu rubutawa (ga ayyuka.)
12. Sunsan abinda kuke aikatawa (dukkansa.)
13. Haƙiƙa su managarta Muminai (wato magasgata a cikin imaninsu) suna cikin aljanna.
14. Haƙiƙa kafirai kuma suna cikin jahannama..
15. Zasu babbake a cikinta a ranar sakamako.
16. Su ba masu fitane ba ga buranta.
17. Menene yasanar dakai ranar sakamako, (girmamawane ga sha'aninsa.)
18. Sannan meye yasanar dakai meye ranar sakamako?
19. Shine ranar da wata kai bazata anfanawa wata kai da komai ba, lamari a wannan rana yana ga Allah.

83 سُورَةُ المُطَفِّفِينَ مَكِّيَّة
وَهِيَ سِتٌّ وَثَلَاثُونَ ءَايَةً 36

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

وَيْلٌ لِّلْمُطَفِّفِينَ ﴿1﴾ اَلَّذِينَ إِذَا اَكْتَالُواْ عَلَى اَلنَّاسِ يَسْتَوْفُونَ ﴿2﴾
وَإِذَا كَالُوهُمْ أَو وَّزَنُوهُمْ يُخْسِرُونَ ﴿3﴾ أَلَا يَظُنُّ أُوْلَٰٓئِكَ أَنَّهُم
مَّبْعُوثُونَ ﴿4﴾ لِيَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿5﴾ يَوْمَ يَقُومُ اُلنَّاسُ لِرَبِّ اِلْعَٰلَمِينَ ﴿6﴾
* كَلَّا إِنَّ كِتَٰبَ اَلْفُجَّارِ لَفِي سِجِّينٍ ﴿7﴾ وَمَا أَدْرَىٰكَ مَا سِجِّينٌ ﴿8﴾ كِتَٰبٌ مَّرْقُومٌ ﴿9﴾ ثمن
وَيْلٌ يَوْمَئِذٍ لِّلْمُكَذِّبِينَ ﴿10﴾ اَلَّذِينَ يُكَذِّبُونَ بِيَوْمِ اِلدِّينِ ﴿11﴾ وَمَا يُكَذِّبُ بِهِۦٓ إِلَّا
كُلُّ مُعْتَدٍ أَثِيمٍ ﴿12﴾ إِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِ ءَايَٰتُنَا قَالَ أَسَٰطِيرُ اُلْأَوَّلِينَ ﴿13﴾ كَلَّا
بَلْ رَّانَ عَلَىٰ قُلُوبِهِم مَّا كَانُواْ يَكْسِبُونَ ﴿14﴾ كَلَّا إِنَّهُمْ عَن رَّبِّهِمْ يَوْمَئِذٍ
لَّمَحْجُوبُونَ ﴿15﴾ ثُمَّ إِنَّهُمْ لَصَالُواْ اُلْجَحِيمِ ﴿16﴾ ثُمَّ يُقَالُ هَٰذَا اَلَّذِي كُنتُم بِهِۦ
تُكَذِّبُونَ ﴿17﴾ كَلَّا إِنَّ كِتَٰبَ اَلْأَبْرَارِ لَفِي عِلِّيِّينَ ﴿18﴾ وَمَا أَدْرَىٰكَ مَا عِلِّيُّونَ ﴿19﴾
كِتَٰبٌ مَّرْقُومٌ ﴿20﴾ يَشْهَدُهُ اُلْمُقَرَّبُونَ ﴿21﴾ إِنَّ اَلْأَبْرَارَ لَفِي نَعِيمٍ ﴿22﴾
عَلَى اَلْأَرَآئِكِ يَنظُرُونَ ﴿23﴾ تَعْرِفُ فِي وُجُوهِهِمْ نَضْرَةَ اَلنَّعِيمِ ﴿24﴾ يُسْقَوْنَ مِن
رَّحِيقٍ مَّخْتُومٍ ﴿25﴾ خِتَٰمُهُۥ مِسْكٌ وَفِي ذَٰلِكَ فَلْيَتَنَافَسِ اِلْمُتَنَٰفِسُونَ ﴿26﴾

Wannan Sura Itace Suratul Tadfifi

A Makka aka saukar da ita aya talatin dashida ce (36)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan Sura ta ƙunshi Fayyacewa ga ba'alin Fajirci misalin Tauye Mudu da ƙaryatawa da Ranar Lahira da shishshigi a kan wanda ya Dangana Alƙur'ani izuwa cewa ƙaryace-ƙaryacen mutane farkone da sababin wannan da Sakamakonsa izuwa Ranar Alƙiyama. sannan Sakamakon managarta. Ita wannan sura sharhice ga surar data gabaceta.)

1. Azabata tabbata ga masu tauye mudu.
2. Waɗanda idan sun auna daga mutane zasu cika mudu.
3. In zasu aunawa mutane da ma'auni saisu tauye awon.
4. Shin waɗancanenka basa tabbatarwar haƙiƙasu za a tashe sune?
5. A cikin rana mai girma.
6. Ranar da mutane suke tashi (daga cikin kaburburansu), saboda sakamakon Ubangijin talikai.
7. Haƙiƙa littafin kafirai fajirai yana cikin Sijjin, (Littafine daya tara aiyukan shaiɗanu da kafirai, wurine a ƙarƙashin ƙasa ta bakwai, garin Iblis da rundunarsa.)
8. Wane abune yasanar dakai meye Littafin Sijjin?
9. Littafi ne abin yumƙewa. |
10. Azaba a wannan rana ta tabbata ga masu ƙaryatawa.
11. Waɗanda suke ƙaryatawa da ranar sakamako.
12. Ba mai ƙaryatawa dashi sai dukkan mai shishshigi mai yawan ɗaukan alhaki.
13. Idan ana karantawa ayoyinmu a gareshi yakance "tatsunuyoyin mutanen farkone".
14. Hir! daga wannan magana, bari abinda suke tsuwurwurta wato suke aikatawa na saboda shine yayi tsatsa a kan zukatansu.
15. Lallai haƙiƙa su ababan tsarewa ne ga buran ganin Ubangijinsu (bazasu ganshi ba.)
16. Sannan haƙiƙa su lallai masu faɗawa cikin wuta ne.
17. Sannan ace dasu "wannan azaba shine wanda kuka kasance kuna ƙaryatawa."
18. Lallai haƙiƙa littafin managarta yana cikin Illiyina, (Littafine mai tarawa da aiyukan alheri na Mala'iku da Muminai a cikin wani guri a sama ƙarƙashin Al'arshi.)
19. Meye yasanar dakai meye Littafin Illiyuna?
20. Littafine abin yumƙewa.
21. Makusanta (na Mala'iku) suna halartarsa.
22. Haƙiƙa managarta lallai suna cikin Aljanna.
23. Suna kan gadajen mulki, suna duban abinda Allah ya basu na ni'ima.
24. Kana sanin garau na jin daɗi a cikin fuskokinsu.
25. Ana sha dasu daga tatacciyar giya abar yumƙewa, (ba mai buɗe yumƙin saisu.)
26. Yumƙin ƙarshensa yana tashin ƙanshin almiski duka mai kwaɗayi yayi kwaɗayi a cikin wancananka, (da garaje izuwa ɗa'ar Allah.)

وَمِزَاجُهُۥ مِن تَسْنِيمٍ (27) عَيْناً يَشْرَبُ بِهَا اَ۬لْمُقَرَّبُونَ (28) إِنَّ اَ۬لذِينَ
أَجْرَمُواْ كَانُواْ مِنَ اَ۬لذِينَ ءَامَنُواْ يَضْحَكُونَ (29) وَإِذَا مَرُّواْ بِهِمْ
يَتَغَامَزُونَ (30) وَإِذَا اَ۟نقَلَبُواْ إِلَيٰ أَهْلِهِمُ اُ۟نقَلَبُواْ فَٰكِهِينَ (31)
وَإِذَا رَأَوْهُمْ قَالُواْ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ لَضَآلُّونَ (32) وَمَا أُرْسِلُواْ عَلَيْهِمْ
حَٰفِظِينَ (33) فَالْيَوْمَ اَ۬لذِينَ ءَامَنُواْ مِنَ اَ۬لْكُفَّارِ يَضْحَكُونَ (34)
عَلَى اَ۬لْأَرَآئِكِ يَنظُرُونَ (35) هَلْ ثُوِّبَ اَ۬لْكُفَّارُ مَا كَانُواْ يَفْعَلُونَ (36)

84 سُورَةُ الانشقاق مَكِّيَّة
وَهِيَ خَمْسٌ وَعِشْرُونَ ءَايَة 25

بِسْمِ اِ۬للَّهِ اِ۬لرَّحْمَٰنِ اِ۬لرَّحِيمِ

إِذَا اَ۬لسَّمَآءُ اُ۟نشَقَّتْ (1) وَأَذِنَتْ لِرَبِّهَا وَحُقَّتْ (2) وَإِذَا اَ۬لْأَرْضُ مُدَّتْ (3)
وَأَلْقَتْ مَا فِيهَا وَتَخَلَّتْ (4) وَأَذِنَتْ لِرَبِّهَا وَحُقَّتْ (5) يَٰٓأَيُّهَا اَ۬لْإِنسَٰنُ
إِنَّكَ كَادِحٌ إِلَيٰ رَبِّكَ كَدْحاً فَمُلَٰقِيهِ (6) فَأَمَّا مَنُ اُ۟وتِيَ
كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ (7) فَسَوْفَ يُحَاسَبُ حِسَاباً يَسِيراً (8) وَيَنقَلِبُ إِلَيٰ أَهْلِهِۦ
مَسْرُوراً (9) وَأَمَّا مَنُ اُ۟وتِيَ كِتَٰبَهُۥ وَرَآءَ ظَهْرِهِۦ (10) فَسَوْفَ يَدْعُواْ
ثُبُوراً (11) وَيَصْلَيٰ سَعِيراً (12) إِنَّهُۥ كَانَ فِي أَهْلِهِۦ مَسْرُوراً (13)

27. Abin tsarmawarsa kuwa na tsanimine.
28. Marmaroce (wato idaniya) da makusanta (ga Allah) suke sha daga gareta.
29. Hakika Wadanda sukayi laifi (kamar Abu Jahil da makamantansa) sun kasance suna dariya ga wadanda suka bada gaskiya (kamar Ammaru da Bilalu da makamantansu.)
30. Suna kifceceniya idan sun wuce garesu (da idanu don izgili.)
31. In sun komo izuwa iyalinsu sukan komo suna masujiji da kai, (saboda ambatonsu Muminai.)
32. In sun ga Muminai sukance hakika wadannan lallai batattune, (Donsun , bada gaskiya da Annabi Sallallahu alaihi wasallama).
33. Ubangiji yace, "ba a aiko kafirai makiyaya a kan Muminai (ko ga aiyukansu ba, ballantana su mai dasu izuwa masalahohinsu).
34. To a yau Wadanda suka bada gaskiya suna dariya daga kafirai.
35. A kan gadaje a cikin aljanna suna duba daga mazaunansu, (izuwa kafirai anayi musu azaba suna kalkyale musu da dariya tamfar da kafirai sukayi musu dariya a duniya.)
36. Yalla a sakawa kafirai abinda suka kasance suna yiwa Mumi nai? (Na'am an saka musu.)

Wannan Sura Itace Suratul Inshikaki

A Makka aka saukar da ita aya ishirin da biyar ce (25)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinkan talikai a duniyagaba daya, mai jinkan Muminai a Lahira a kebe.

(Wannan sura ta kunshi Mukaddamom Ranar Alkiyama sannan Matukar kowane mutum da abinda zai kasance kansa Ranar Alkiyama sannan rantsuwa da Shafaki da Dare da Wata, lallai zaku kasance a cikin Rayuwa ta biyu da zata zama kamar ta farko, sannan musu a garesu saboda rashin Imani da karyatawarsu.)

1. Idan sama ta kece.
2. Ta saurari Ubangijinta ta bishi a cikin kecewa, an wajabta mata,taji, tabi
3. Idan kasa akayi kari a cikin yalwarta, (ba gini ba dutse a kanta.)
4. Ta fitar da abinda yake cikinta (na matattu izuwa bayanta,) ta wofintu (ga buranta.)
5. Ta saurari Ubangijinta tabishi a cikin haka alhali wajibine tajishi tabishi, (wancenenka dukkaninsa yana kasancewa ranar alkiyama, jawabin; a rannan mutum zai gamu da aikinsa.)
6. Ya kai wannan mutum, hakika kai mai wahala ne a cikin aikinka izuwa gamo da Ubangijinka, wahala, to zaka sadu da sakamakon aikinkane (na hairi ko sharri a ranar alkiyama, wato zai dandana kudarsa.)
7. To amma wanda aka bashi takardar aikinsa a hannun damansa (Shine Mumini).
8. Da sannu za ayi masa sakamako, sakamako mai sauki (Shine bijirar da aikinsa a gareshi, (kamar da aka fassara a Hadisin Sahihaini , a cikinsa: wanda akayi masa munakashar Hisabi ya halaka; to bayan bijirar wannan sai ayi masa rangwame.)
9. Yakoma izuwa iyalinsa mai farin ciki, (cikin Aljanna.)
10. Amma wanda aka bashi Litafinsa ta bayan bayansa (Shine kafiri, a kukunce damasa izuwa wuyansa, a mai da hagun dinsa a bayansa ya riki takardasa da ita.)
11. Da sannu zaiyi kiran ya halakarsa (yayin ganin abinda yake cikinsa.)
12. Zai fada wutar Sa'ira.
13. Hakika ya kasance a cikin iyalinsa (a duniya) yana murna (ta shakiyanci ya biyewa son ransa.)

ربع

إِنَّهُۥ ظَنَّ أَن لَّن يَحُورَ ﴿14﴾ بَلَىٰٓ إِنَّ رَبَّهُۥ كَانَ بِهِۦ بَصِيرًا ﴿15﴾ * فَلَآ أُقْسِمُ
بِالشَّفَقِ ﴿16﴾ وَالَّيْلِ وَمَا وَسَقَ ﴿17﴾ وَالْقَمَرِ إِذَا اَتَّسَقَ ﴿18﴾ لَتَرْكَبُنَّ طَبَقًا
عَن طَبَقٍ ﴿19﴾ فَمَا لَهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿20﴾ وَإِذَا قُرِئَ عَلَيْهِمُ الْقُرْءَانُ لَا يَسْجُدُونَ ﴿21﴾
بَلِ الَّذِينَ كَفَرُوا يُكَذِّبُونَ ﴿22﴾ وَاللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا يُوعُونَ ﴿23﴾
فَبَشِّرْهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿24﴾ إِلَّا الَّذِينَ ءَامَنُوا وَعَمِلُوا الصَّٰلِحَٰتِ لَهُمُ أَجْرٌ غَيْرُ مَمْنُونٍ ﴿25﴾

سُورَةُ الْبُرُوجِ مَكِّيَّةٌ 85

وَهِيَ ثِنْتَانِ وَعِشْرُونَ ءَايَةً 22

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

وَالسَّمَآءِ ذَاتِ الْبُرُوجِ ﴿1﴾ وَالْيَوْمِ الْمَوْعُودِ ﴿2﴾ وَشَاهِدٍ وَمَشْهُودٍ ﴿3﴾
قُتِلَ أَصْحَٰبُ الْأُخْدُودِ ﴿4﴾ النَّارِ ذَاتِ الْوَقُودِ ﴿5﴾ إِذْ هُمْ عَلَيْهَا قُعُودٌ ﴿6﴾
وَهُمْ عَلَىٰ مَا يَفْعَلُونَ بِالْمُؤْمِنِينَ شُهُودٌ ﴿7﴾ وَمَا نَقَمُوا مِنْهُمْ إِلَّا أَن يُؤْمِنُوا
بِاللَّهِ الْعَزِيزِ الْحَمِيدِ ﴿8﴾ الَّذِى لَهُۥ مُلْكُ السَّمَٰوَٰتِ وَالْأَرْضِ وَاللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ
شَىْءٍ شَهِيدٌ ﴿9﴾ إِنَّ الَّذِينَ فَتَنُوا الْمُؤْمِنِينَ وَالْمُؤْمِنَٰتِ ثُمَّ لَمْ يَتُوبُوا فَلَهُمْ
عَذَابُ جَهَنَّمَ وَلَهُمْ عَذَابُ الْحَرِيقِ ﴿10﴾ إِنَّ الَّذِينَ ءَامَنُوا وَعَمِلُوا الصَّٰلِحَٰتِ
لَهُمْ جَنَّٰتٌ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَٰرُ ذَٰلِكَ الْفَوْزُ الْكَبِيرُ ﴿11﴾

14. Haƙiƙa shiya zaci bazai koma izuwa Ubangijinsa ba.
15. A'a yakoma izuwa Ubangijinsa, haƙiƙa Ubangijinsa ya kasance masani dashi.
16. To ina rantsuwa da shafaƙi (ja wanda yake kamar gantako bayan faɗuwar rana.)
17. Ya rantse da dare da wanda ya tara (na daga dabbobi da waninsa.)
18. Ya rantse da wata idan ya cika fararen darare.
19. Wallahi zaku hau hali bayan hali (Shine mutuwa, sannan rayuwa da abinda Yake bayanta na daga haluluwan alƙiyama.)
20. To meke garesune basa bada gaskiya (tareda samun hujjoji a gareshi?).
21. Meke garesu in an karanta musu Alƙur'ani basa sujada, (ya zama saboda gasgatawa.)
22. Bari! wadanda suka kafirta suna ƙaryatawa da tashin alƙiyama.
23. Allah ne masani da abinda suke tarawa (cikin takardunsu na kafirci da ƙaryatawa, da miyagun aiyuka).
24. Kayi musu albishir da azaba mai raɗ aɗi.
25. Sai Waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki na gari, lada ba abin yankewa ba yana garesu, (bazai musu gori dashi ba.)

Wannan Sura Itace Suratul Buruji taurari goma sha buyu

A Makka aka saukar da ita aya ishirin da biyuce (22)

Ina farawa dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan Sura ta ƙunshi Rarrashin Ma'aikin Allah Sallallahu alihi wasallama da Muminai da ƙarfafansu a kan cutar mutanensu, sannan 'ta sanya musu misalce-misalce da Ashabul Uhdudi da Fir'auna da sanyaya zukatan Muminai da Bayanin ƙarshen kafirai dana Muminai da Ambaton Alƙur'ani a ƙarshenta.)

1. Ubangiji ya rantse da sama ma'abucuyar burujai goma sha biyu.
2. Ya rantse da ranar abin alƙawartawa shine Alƙiyama Saboda Allah ya alƙawarta Zuwansa.
3. Da ranar juma'a Saboda yawan shaidawa da aiki a cikinsa, da ranar Arfa Saboda Motane da Mala'iku Suna halartarsa. (Jawabin rantsuwa).
4. Wallahi an la'anci ma'abota gwalalo.
5. Wuta ma'abociyar huruwa (gasu sune gumagumanta).
6. A zamanin dasu suke zaune a daura da gwalalon.

(MUMINAN FARKO SUNFIMU ƘARFIN RAI BISA BADA GASKIYA DA ALLAH.)

7. Suna duban abindasu suke aikatawa da Muminai (Shine yi musu azabar da jefasu a cikin wuta in basu komao ga buran imaninsu ba, an ruwaito cewa haƙiƙa Allah ya tserar da Muminai Waɗanda aka jefa a cikin wutar nan da karɓar rayukansu tun gaban basu faɗa cikinta ba, wato tun gaban faɗawa wutar, wutar ta fito waje ta ƙonesu masu jefa Muminai.)
8. Basu ƙi komai daga garesu basai kawaisu bada gaskiya da Allah mabuwayi (cikin mulki,) abin godewa (cikin aiki.)
9. Wanda mulkin sammai da ƙassai yake gareshi, Allah mai dubane ga kowane abu. Ai kafirai basuyi musun komai ga Muminai basai (Manin da sukayi da Allah).
10. Haƙiƙa waɗanda suka fitunci Muminai maza da mata (da konewa) sannan basu tuba ba, to azabata Jahannama na garesu, (saboda kafircinsu,) azaba mai tsananin zafi na garesu.
11. Haƙiƙa waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru aljannatai na garesu, wannan Shine rabo mai girma.

ثمن

* إِنَّ بَطْشَ رَبِّكَ لَشَدِيدٌ ﴿12﴾ إِنَّهُۥ هُوَ يُبْدِئُ وَيُعِيدُ ﴿13﴾
وَهُوَ الْغَفُورُ الْوَدُودُ ﴿14﴾ ذُو الْعَرْشِ الْمَجِيدُ ﴿15﴾ فَعَّالٌ لِّمَا يُرِيدُ ﴿16﴾
هَلْ أَتَىٰكَ حَدِيثُ الْجُنُودِ ﴿17﴾ فِرْعَوْنَ وَثَمُودَ ﴿18﴾ بَلِ الَّذِينَ
كَفَرُوا فِي تَكْذِيبٍ ﴿19﴾ وَاللَّهُ مِن وَرَآئِهِم مُّحِيطٌ ﴿20﴾
بَلْ هُوَ قُرْءَانٌ مَّجِيدٌ ﴿21﴾ فِي لَوْحٍ مَّحْفُوظٍ ﴿22﴾

86 سُورَةُ الطَّارِقِ مَكِّيَّةٌ
وَهِيَ سِتَّ عَشْرَةَ ءَايَةً 16

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

وَالسَّمَآءِ وَالطَّارِقِ ﴿1﴾ وَمَا أَدْرَىٰكَ مَا الطَّارِقُ ﴿2﴾ النَّجْمُ الثَّاقِبُ ﴿3﴾
إِن كُلُّ نَفْسٍ لَّمَّا عَلَيْهَا حَافِظٌ ﴿4﴾ فَلْيَنظُرِ الْإِنسَانُ مِمَّ خُلِقَ ﴿5﴾
خُلِقَ مِن مَّآءٍ دَافِقٍ ﴿6﴾ يَخْرُجُ مِنۢ بَيْنِ الصُّلْبِ وَالتَّرَآئِبِ ﴿7﴾
إِنَّهُۥ عَلَىٰ رَجْعِهِۦ لَقَادِرٌ ﴿8﴾ يَوْمَ تُبْلَى السَّرَآئِرُ ﴿9﴾ فَمَا لَهُۥ مِن قُوَّةٍ وَلَا نَاصِرٍ ﴿10﴾
وَالسَّمَآءِ ذَاتِ الرَّجْعِ ﴿11﴾ وَالْأَرْضِ ذَاتِ الصَّدْعِ ﴿12﴾ إِنَّهُۥ لَقَوْلٌ
فَصْلٌ ﴿13﴾ وَمَا هُوَ بِالْهَزْلِ ﴿14﴾ إِنَّهُمْ يَكِيدُونَ كَيْدًا
وَأَكِيدُ كَيْدًا ﴿15﴾ فَمَهِّلِ الْكَٰفِرِينَ أَمْهِلْهُمْ رُوَيْدًا ﴿16﴾

12. Haƙiƙa riƙon Ubangijinka (da kafirci) lallai mai tsanani ne.
13. Haƙiƙa lamarin shi mai tsananin nufine ya maida farin halitta bayan sun mutu.
14. Shine mai gafara (ga Muminai.) Shine mai soyuwa (da waliyansa da karama.)
15. Mahaliccin Al'arshi mai girma.
16. Mai aikata abinda yakeso.
17. Labarin runduna yazo maka (ya Muhammadu Sallallahu alaika wasallama?).
18. Fir'auna da Samadu, (labarinsu su cewa an halakar dasu da katircinsu, wannan faɗakarwanc ga wanda ya bada gaskiya da Annabi Sallallahu alaihi wasal-lama da Alƙur'ani domin su wa'azantu.)
19. Bari! har yanzu dai waɗanda suka kafirta suna cikin Ƙaryatawa (da ayoyin Allah.)
20. Allah mai kewayewa ne dasu, (ba mai kiyayesu daga gareshi.)
21. Bari! shi Alƙur'anine mai girmane (a sama ta bakwai.)
22. A cikin Allo (wanda yake cikin hawa burbushi sama ta bakwai, ba mai taɓa shi daga mutane da aljanna,) abin kiyayewa (daga shaiɗani da jirkitar wani abu daga gareshi tsawonsa abinda yake tsakanin sama da ƙasa faɗinsa abinda yake tsakanin mahudar rana da mafaɗarta daga. Lu'ulu'anya fara yake (Ibn. Abbas radhiyallalu anhu shi yafaɗeshi.)

Wannan Sura Itace Suratu Ɗariki

A Makka aka saukar da ita aya goma sha bakwai ce (17)

Ina fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan Sura tayi magana a kan kowane mutum yana da mai kiwo da yake kiyaye shi Shine Allah da dalili a kan wannan sannan tabbatar da tashi sannan ta cika da zance kan Alƙur'ani da kaidin kafirai da mushurkai da gasgata ma'aikin Allah Sallaltahu alaihi wasallama.)

1. Ubangiji ya rantse da sama da tauraro mai suna Ɗariku (duk mai zuwa da dare sunansa ɗariku saboda hakane aka sawa waɗannan taurari Ɗariku don saida dare suke fitowa).
2. Menene yasanar dakai meye ɗariku (anyi wannan ibara don girmama Sha'anin ɗariku.)
3. Tauraro ne mai tsananin haske, (ko dukkan tauraro mai huda duhu da haskensa.)
4. (Jawabin rantsuwa) haƙiƙa lamarin da Sha'anin kowace kai lallai mai kiwo yana kanta (na Mala'iku da yake kiyaye aikinta na hairi ko sharri da izinin Allah.)
5. To mutum yayi tunani daga me ake halicce shi?
6. An halicce shi daga ruwa mai izo (daga namiji, mai izo daga mace a cikin mahaifarta.)
7. Yana fita daga tsatson namiji (wato ƙasusuwan baya) da karankarmu (na mace wato ƙasusuwan ƙirjinta.)
8. Ubangiji lallai mai ikone bisa tashin mutum bayan ya mutu.
9. Ranar da ake jarrabar asirin bayi, (ƙudure-ƙudure da niyoyi.)
10. Bashi da wani ƙarfi (dazai hanawa kansa azaba) wala mai taimako (dazai ije masa ita.)
11. Allah ya rantse da sama ma'abociyar zubar da ruwa, (Ance dashi raj'u saboda komawarsa kowane lokaci.)
12. Ya rantse da ƙasa ma'abuciyar tsagewa (da tsiri.)
13. Haƙiƙa Alƙur'ani maganace mai rarrabewa (tsakanin ƙarya da gaskiya.)
14. Shi bai kasance tumasanci ba, (wato wasanni.)
15. Haƙiƙasu kafirai suna kaidi (ga Ma'aikin Allah (Sallallahu alaihi wasallama) Kaidi.. Ni kuma ina shirya musu sakamakon kaidin (wato maƙarƙashiya ta inda basu sani ba.)
16. Ka yiwa kafirai sauraro (ya Annabi Sallallahu alaihi wasallama) kayi masu sauraro kaɗan (allah ya kamasu a badar, an shafe sauraron da Ayatussaifi.

حزب

سُورَةُ الْأَعْلَىٰ مَكِّيَّةٌ 87

وَهِيَ تِسْعَ عَشْرَةَ ءَايَةً 19

بِسْمِ اِللَّهِ اِلرَّحْمَٰنِ اِلرَّحِيمِ

* سَبِّحِ اِسْمَ رَبِّكَ اَلْأَعْلَى (1) اَلَّذِے خَلَقَ فَسَوَّىٰ (2) وَالَّذِے قَدَّرَ فَهَدَىٰ (3)
وَالَّذِے أَخْرَجَ اَلْمَرْعَىٰ (4) فَجَعَلَهُۥ غُثَآءً اَحْوَىٰ (5) سَنُقْرِئُكَ فَلَا تَنسَىٰٓ (6)
إِلَّا مَا شَآءَ اَللَّهُ إِنَّهُۥ يَعْلَمُ اُلْجَهْرَ وَمَا يَخْفَىٰ (7) وَنُيَسِّرُكَ لِلْيُسْرَىٰ (8)
فَذَكِّرِ اِن نَّفَعَتِ اِلذِّكْرَىٰ (9) سَيَذَّكَّرُ مَنْ يَّخْشَىٰ (10) وَيَتَجَنَّبُهَا اَلْأَشْقَى (11)
اَلَّذِے يَصْلَى اَلنَّارَ اَلْكُبْرَىٰ (12) ثُمَّ لَا يَمُوتُ فِيهَا وَلَا يَحْيَىٰ (13) قَدْ أَفْلَحَ مَن تَزَكَّىٰ (14)
وَذَكَرَ اَسْمَ رَبِّهِۦ فَصَلَّىٰ (15) بَلْ تُوثِرُونَ اَلْحَيَوٰةَ اَلدُّنْيَا (16) وَالْأخِرَةُ خَيْرٌ
وَأَبْقَىٰٓ (17) إِنَّ هَٰذَا لَفِے اِلصُّحُفِ اِلْأُولَىٰ (18) صُحُفِ إِبْرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ (19)

سُورَةُ الْغَاشِيَةِ مَكِّيَّةٌ 88

وَهِيَ سِتٌّ وَعِشْرُونَ ءَايَةً 26

بِسْمِ اِللَّهِ اِلرَّحْمَٰنِ اِلرَّحِيمِ

هَلْ أَتَىٰكَ حَدِيثُ اُلْغَٰشِيَةِ (1) وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ خَٰشِعَةٌ (2) عَامِلَةٌ نَّاصِبَةٌ (3)
تَصْلَىٰ نَارًا حَامِيَةً (4) تُسْقَىٰ مِنْ عَيْنٍ ـانِيَةٍ (5) لَّيْسَ لَهُمْ طَعَامٌ اِلَّا مِن ضَرِيعٍ (6)

Wannan Sura Itace Suratul A'ala

A Makka aka saukar da ita aya goma sha tara ce (19)

Ina fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan Sura ta ƙunshi Umarni da Tasbihi da Tsarkakewa sannan umarni da gargaɗi sannan Tsira ya tabbata ga wanda ya tsarkake kansa ga buran saɓon Allah da son duniya, Annabi Sallallahu alaihi wasallama yana son wannan sura don abinda ta ƙunsa na daga Sannai da Alhairai.)

1. Tsarkake sunan Ubangijinka mafi ɗaukaka (ga buran abinda bai kamace shi ba.)
2. Wanda ya halicci (mutum) ya daidaita (halitarsa Ya sanyashi mai dacewar juzu'ai ba mai saɓawar juzu'ai ba). **3.** Wanda ya ƙaddara abinda yaga dama ya shiryi (kowa izuwa abinda ya ƙaddara masa na hairi ko sharri.) **4.** Wanda yafitar da makiyaya. **5.** Ya sanyashi bayan korentaka tattaka baƙiƙirin ƙeƙashashahe.
6. Da sannu zamu karanta maka (Alƙur'ani) bazaka manta (abinda kake karantashi ba.)
7. Sai abinda allah yanufi (ka mantashi da shafe karatunsa da hukuncinsa. Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama ya kasance yana kamar an nufi bayyana wada karatu tane da karatun Jibrila Alaihissalamu don gudun Mantuwace dashi kar kayi gaggawa dashi kai bazaka mance dashi ba, kadaka wahalar da kanka da baiyanawa da karuta.) Haƙiƙa Ubangiji yasan baiyanawar magana da aiki da abinda yake ɓuya (daga garesu.)
8. Zamu hore (halittarka) saboda shari'a mai sauƙi (Itace Musulunci.)
9. Kayi gargaɗi (da Alƙur'ani) in gargaɗin zaiyi anfani, (yana nufin koda bazaiyi anfani ba, anfaninta ga ba'ali, rashin anfanin ga ba'ali ne kuma amma wannan ya keɓanci Ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wasallama.)
10. Da sannu wanda yake tsoron Allah zai gargaɗu (da ita.) **11.** Kafirai kuma zai nisanceta.
12. Wanda yake faɗawa wuta mafi girma (Itace wutar lahira, wutar duniya Itace ƙarama.)
13. Sannan bazai mutu a cikinta ba (ballantana ya huta,) kuma bazai rayu (rayuwar da zata amfane shi) ba. **14.** Haƙiƙa wanda ya tsarkaka (da imani) ya rabauta.
15. Ya ambaci Ubangijinsa (yana mai cewa Allahu akbar,) ya sallaci (sallah biyar, wannan yana daga aiyukan Lahira; kafiran Makka kuwa ba ruwansu da wannan.)
16. Barı! Kuna fifita rayuwar duniya (a kan Lahira.)
17. Lahira kuwa (wacce ta ƙunshı anfanin duniya da Lahira,) tafi anfani, kuma tafi wanzuwa.
18. haƙiƙa wannan (rabauta da wannan tsarkakewa da kasancewar Lahira tafi,) lallai suna cikin littattafai na farko (wadanda aka saukar gaban Alƙur'ani.)
19. Littattafan Annabi Ibrahima da Annabi Musa (goma na Annabi Ibrahim, Attaura ta Annbi Musa alaihimassalamu.)

Wannan Sura Itace Suratul Gashiya

A Makka aka saukar da ita aya ishrin dashida ce (26)

Ina fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan Sura ta tattarar a kan Mai lulluɓewa da tsoro da kuma mutane kashi biyune da ba'alin Ikon Allah, da umarnin Annabi Sallallahu alaihi wasallama dayin gargaɗi da cewa kuma komai izuwa Allah zai koma.)

1. Haƙiƙa labarin Mai Lulluɓewa da tsarmakatanta yazo maka.
2. Fuskoki wannan rana wulaƙantattu ne.
3. Masu aiki tuƙuru (cikin sarƙoƙi da ƙuƙumai)masu wahala.
4. Zata faɗa wuta mai tsanannin ƙuna.
5. Za a sha da ita daga idaniya mai tsananin zafi.
6. Basu da abinci sai daga ƙaya (wato ƙaya mummuna wacce dabba bata cinta.)

لَا يُسْمِنُ وَلَا يُغْنِي مِن جُوعٍ ﴿7﴾ وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ نَّاعِمَةٌ ﴿8﴾ لِّسَعْيِهَا رَاضِيَةٌ ﴿9﴾
فِي جَنَّةٍ عَالِيَةٍ ﴿10﴾ لَّا تَسْمَعُ فِيهَا لَاغِيَةً ﴿11﴾ فِيهَا عَيْنٌ جَارِيَةٌ ﴿12﴾ فِيهَا
سُرُرٌ مَّرْفُوعَةٌ ﴿13﴾ وَأَكْوَابٌ مَّوْضُوعَةٌ ﴿14﴾ وَنَمَارِقُ مَصْفُوفَةٌ ﴿15﴾ وَزَرَابِيُّ
مَبْثُوثَةٌ ﴿16﴾ * أَفَلَا يَنظُرُونَ إِلَى الْإِبِلِ كَيْفَ خُلِقَتْ ﴿17﴾ وَإِلَى السَّمَاءِ كَيْفَ
رُفِعَتْ ﴿18﴾ وَإِلَى الْجِبَالِ كَيْفَ نُصِبَتْ ﴿19﴾ وَإِلَى الْأَرْضِ كَيْفَ سُطِحَتْ ﴿20﴾ فَذَكِّرْ
إِنَّمَا أَنتَ مُذَكِّرٌ ﴿21﴾ لَّسْتَ عَلَيْهِم بِمُصَيْطِرٍ ﴿22﴾ إِلَّا مَن تَوَلَّىٰ وَكَفَرَ ﴿23﴾ فَيُعَذِّبُهُ اللَّهُ
الْعَذَابَ الْأَكْبَرَ ﴿24﴾ إِنَّ إِلَيْنَا إِيَابَهُمْ ﴿25﴾ ثُمَّ إِنَّ عَلَيْنَا حِسَابَهُم ﴿26﴾

ثمن

89 سُورَةُ الفَجْرِ مَكِّيَّةٌ

وَهِيَ ثِنْتَانِ وَثَلَاثُونَ ءَايَةً 32

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

وَالْفَجْرِ ﴿1﴾ وَلَيَالٍ عَشْرٍ ﴿2﴾ وَالشَّفْعِ وَالْوَتْرِ ﴿3﴾ وَاللَّيْلِ إِذَا يَسْرِ ﴿4﴾ هَلْ
فِي ذَٰلِكَ قَسَمٌ لِّذِي حِجْرٍ ﴿5﴾ أَلَمْ تَرَ كَيْفَ فَعَلَ رَبُّكَ بِعَادٍ ﴿6﴾ إِرَمَ ذَاتِ الْعِمَادِ ﴿7﴾
الَّتِي لَمْ يُخْلَقْ مِثْلُهَا فِي الْبِلَادِ ﴿8﴾ وَثَمُودَ الَّذِينَ جَابُوا
الصَّخْرَ بِالْوَادِ ﴿9﴾ وَفِرْعَوْنَ ذِي الْأَوْتَادِ ﴿10﴾ الَّذِينَ طَغَوْا فِي الْبِلَادِ ﴿11﴾
فَأَكْثَرُوا فِيهَا الْفَسَادَ ﴿12﴾ فَصَبَّ عَلَيْهِمْ رَبُّكَ سَوْطَ عَذَابٍ ﴿13﴾ إِنَّ رَبَّكَ لَبِالْمِرْصَادِ ﴿14﴾

7. Baya kiƙantarwa baya wadatarwa (daga yunwa.)
8. Da fuskoki mani'imta a wannan rana.
9. Mai yada da aikinta (a duniya da aikinta na ɗa'a, da sakamako a cikin Lahira.)
10. A cikin Aljanna maɗaukakiya (a zahiri da baɗini.)
11. Ba a jin wata kai mai zancen banza a cikinta.
12. Akwai idaniya mai gudana cikinta.
13. Da gadaje ababan ɗaukakawa (a Zati da alƙadari da mahalli.)
14. Da funjalai marasa maɗauki a gefen idanduna.
15. Da matasan kai ababan jerawa, ba'ali kan ba'ali, (kamar yadda mutanen Makka suke aikatawa izuwa yau).
16. Da kilisai ababan shinfiɗawa.
17. Shin basa duba izuwa raƙuma, yaya aka halicce ta?.
18. Kai duba izuwa sama yaya aka ɗaukakata?.
19. Kai duba izuwa duwarwatsu yaya aka kafata?.
20. Kai duba izuwa ƙasa yaya aka shimfiɗeta? (Ko da yake a haƙiƙa kamar tamaula take a zahiri a shimfiɗe take. Ku kafa dalili 'da ita izuwa ikon Allah, an fara da raƙuma saboda su sunfi tsananin cuɗanya da ita..)
21. Kayi musu gargaɗi (da ni'imomin Allah da dalilan tauhidi nasa) kai dai kawai mai gargaɗi ne.
22. Baka kasance mai tilasta ne a kansu ba.
23. Sai wanda ya juya baya (ga buran Alƙur'ani) saiya karfice (da Alƙur'ani.)
24. To Allah zaiyi masa azaba mafi girma (azabar lahira da karama ta duniya, kisa da ribacewa.)
25. Haƙiƙa garemune komawarsu (bayan mutuwa.)
26. Sannan haƙiƙa sakamakonsu yana kanmu (bazamu barsu ba har abada.)

Wannan Sura Itace Suratul Fajri

a Makka aka saukar da ita aya talatin da biyuce (32)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan Sura ta tattarar bisa Rantsuwa a kan kafirai za ayi musu Azaba tamƙar daza a yiwa waɗansu daga al'umomi da suka wuce da bayanin mutum da ɗabi'arsa da bayanin matsayinsa ranar Alƙiyama.)

1. Ubangiji ya rantse da Alfijir ɗin kowace rana.
2. Da daren goma na zilhijjati.
3. Da cika da mara.
4. Da dare idan ya tafi yagabato koya bada baya.
5. Akwai rantsuwa ga masu hankali da wancanenka rantsuwa (jawabin rantsuwa, Wallahi za ayi muku azabaya kafiran Makka.)
6. Shin baka sani ba (Ya Annabi Sallallahu alihi wasallama) yaya Ubangijinka ya aikata da Ãdu?
7. Itace iramu, ma'abociyar tsawo kamar ginshiƙi.
8. Wacce ba a halicci irinta ba a garuruwa, (a cikin damƙa da ƙarfin jiki (labarin da aka bayar mai tsawo kamar zira'i dari huɗu (400) an gabatar dashi.)
9. Da Samudu wadanda suka yanke fa, (suka riƙeta ɗakuna,) a Wadil Kura.
10. Da fir'auna ma'abocin turaku, (yakan kafa turke guda huɗu, ya ɗaure hannaye da ƙafafu na wanda yake masa azaba.)
11. Waɗanda sukayi shishshigi a cikin garuruwa.
12. Suka yawaita ɓarna a garuruwa, (kisa da waninsa.)
13. Sai Ubangijinka ya zuba musu nau'in azaba.
14. Haƙiƙa Ubangijinka yana madakata (ta aikin bayi bazasu tsere masa ba.)

فَأَمَّا ٱلْإِنسَٰنُ إِذَا مَا ٱبْتَلَىٰهُ رَبُّهُۥ فَأَكْرَمَهُۥ وَنَعَّمَهُۥ ﴿15﴾ فَيَقُولُ رَبِّيَ
أَكْرَمَنِ ﴿16﴾ وَأَمَّا إِذَا مَا ٱبْتَلَىٰهُ فَقَدَرَ عَلَيْهِ رِزْقَهُۥ ﴿17﴾ فَيَقُولُ رَبِّيَ
أَهَٰنَنِ ﴿18﴾ كَلَّا بَل لَّا تُكْرِمُونَ ٱلْيَتِيمَ ﴿19﴾ وَلَا تَحَٰضُّونَ عَلَىٰ طَعَامِ
ٱلْمِسْكِينِ ﴿20﴾ وَتَأْكُلُونَ ٱلتُّرَاثَ أَكْلًا لَّمًّا ﴿21﴾ وَتُحِبُّونَ ٱلْمَالَ حُبًّا جَمًّا ﴿22﴾
كَلَّا إِذَا دُكَّتِ ٱلْأَرْضُ دَكًّا دَكًّا ﴿23﴾ وَجَآءَ رَبُّكَ وَٱلْمَلَكُ صَفًّا صَفًّا ﴿24﴾
وَجِاْيٓءَ يَوْمَئِذٍ بِجَهَنَّمَ ﴿25﴾ يَوْمَئِذٍ يَتَذَكَّرُ ٱلْإِنسَٰنُ وَأَنَّىٰ لَهُ ٱلذِّكْرَىٰ ﴿26﴾
يَقُولُ يَٰلَيْتَنِي قَدَّمْتُ لِحَيَاتِي ﴿27﴾ فَيَوْمَئِذٍ لَّا يُعَذِّبُ عَذَابَهُۥٓ أَحَدٌ ﴿28﴾
وَلَا يُوثِقُ وَثَاقَهُۥٓ أَحَدٌ ﴿29﴾ يَٰٓأَيَّتُهَا ٱلنَّفْسُ ٱلْمُطْمَئِنَّةُ ﴿30﴾
ٱرْجِعِيٓ إِلَىٰ رَبِّكِ رَاضِيَةً مَّرْضِيَّةً ﴿31﴾ فَٱدْخُلِي فِي عِبَٰدِي وَٱدْخُلِي جَنَّتِي ﴿32﴾

سُورَةُ الْبَلَدِ مَكِّيَّةٌ 90
وَهِيَ عِشْرُونَ ءَايَةً 20

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

* لَآ أُقْسِمُ بِهَٰذَا ٱلْبَلَدِ ﴿1﴾ وَأَنتَ حِلٌّۢ بِهَٰذَا ٱلْبَلَدِ ﴿2﴾ وَوَالِدٍ وَمَا وَلَدَ ﴿3﴾ ربع
لَقَدْ خَلَقْنَا ٱلْإِنسَٰنَ فِي كَبَدٍ ﴿4﴾ أَيَحْسِبُ أَن لَّن يَقْدِرَ عَلَيْهِ أَحَدٌ ﴿5﴾
يَقُولُ أَهْلَكْتُ مَالًا لُّبَدًا ﴿6﴾ أَيَحْسِبُ أَن لَّمْ يَرَهُۥٓ أَحَدٌ ﴿7﴾

15. Amma mutum kafiri idan Ubangijinsa ya jarrabe shi (da dukiya da waninta) ya ni'imtashi.
16. Yana cewa "Ubangijina ya girmama ni
17 . Amma idan ya jarrabe shi yaƙuntata arzikinsa a gareshi.
18. Ya kance "Ubangijina ya wulaƙantani".
19. Hir! (Ku dama wannan magana, girmamawa ba daga dukiya bane, wulaƙantawa bada taulauci bane, shidai ɗa'ane ga Allah da saɓon Allah, mutane basu kula da wannan ba.) Bari! basa girmama maraya (tareda wadatarsu, basa bashi haƙƙinsa na gado.)
20. Bakwa kwaɗaitar da kanku ko waninku a kan ciyar da miskini.
21. Kuna cin dukiyar marayaci na hayamhayam.
22. Kuna son tara ɗinbin dukiyaso mai yawa.
23. Hir! ga buran wannan, Idan aka dandaƙe ƙasa dandaƙewa (duk ginin da yake kanta ya rushe.)
24. Al'amarin Ubangijinka yazo da Mala'iku safusafu.
25. Aka zoda Jahannama (a wannan rana ana jan tada ragama dubu •saba'in a hannun Mala'iku dubu saba'in, tana ƙaragi da rugugi.)
26. A wannan ranane kafiri zai tuna (abinda yayi sakaci a duniya,) ina anfanin tunawa gareshi (a wannan lokaci?).
27. Zaice (tareda wannan tunawar) "kaico! daya kace ni na gabatar da alheri da imani a cikin rayuwata daddada a lahira tun ina duniya."
28. A wannan rana ba ɗaya dazaiyi azaba irin azabar Allah, bakuma zai wakkala azabar izuwa wani ba.
29. Wani bazai tamƙe kafiri irin tamƙewarsa ba.
30. Yake wannan kai wacce ta nutsu (da imani da Allah.)
31. (Ana cewa da ita) "Koma izuwa Ubangijinki (umarninsa da nufinsa,) kina mai yarda (da sakamakonsa,) kina abar yarda (nan ga Ubangiji ga aikin ki na gari".)
32. (Ana cewa da ita ranar Alƙiyama "To shiga cikin jumlar bayi managarta •ki shiga aljannata (tare dasu".)

Wannan Itace Suratul Baladi

A Makka aka saukar da ita aya ishirin ce (20)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

Wannan Sura ta ƙunshi Rantsuwa a kan wahala da cewa ruɗaɗɗe wato kaladalu ɗan Aidu aljanali yana zaton ba mai iko a kansa, sannan bayanin Ni'imomin Allah ga mutum sannan kiransa izuwa kutsa tsauni tareda bayanin 'yan Dama da 'yan Hauni.)

1. Ubangiji yana rantsuwa da wannan gari Makka.
2. Ya sai Annanbi (Sallallahu alaihi wasallama) kana halali (wato maras harama jiki) a wannan gari (Shine ya halatta gareka kayi yaƙi a cikinsa Allah ya danƙa masa wannan alƙawarin ranar buɗe Makka, wannan jimlar' tashiga tsakanin abin rantsuwa dashi da abinda aka ɗora a kansa).
3. Ina rantsuwa da mahaifi (Annabi Adamu Alaihissalamu) da abinda ya haifa (sune zurriyarsa.)
4. Wallahi mun halicci mutum a cikin wahala; (musibun duniya dana lahira.)
5. Saboda me (ƙaƙƙarfan ƙuraishu kaladata ɗan Usaidu) zai zaci cewa bamai iko a kansa. (Allah mai ikone a kansa.)
6. Yana cewa ya halakar da dukiya mai yawa (a kan gabada Annabi Sallallahu alaihi wasallama.)
7. Shin yana zaton bamai ganinsa?

أَلَمْ نَجْعَل لَّهُۥ عَيْنَيْنِ ﴿8﴾ وَلِسَانًا وَشَفَتَيْنِ ﴿9﴾ وَهَدَيْنَٰهُ ٱلنَّجْدَيْنِ ﴿10﴾
فَلَا ٱقْتَحَمَ ٱلْعَقَبَةَ ﴿11﴾ وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا ٱلْعَقَبَةُ ﴿12﴾ فَكُّ رَقَبَةٍ ﴿13﴾
أَوْ إِطْعَٰمٌ فِى يَوْمٍ ذِى مَسْغَبَةٍ ﴿14﴾ يَتِيمًا ذَا مَقْرَبَةٍ ﴿15﴾ أَوْ مِسْكِينًا
ذَا مَتْرَبَةٍ ﴿16﴾ ثُمَّ كَانَ مِنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَتَوَاصَوْا۟ بِٱلصَّبْرِ
وَتَوَاصَوْا۟ بِٱلْمَرْحَمَةِ ﴿17﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْمَيْمَنَةِ ﴿18﴾ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟
بِـَٔايَٰتِنَا هُمْ أَصْحَٰبُ ٱلْمَشْـَٔمَةِ ﴿19﴾ عَلَيْهِمْ نَارٌ مُّؤْصَدَةٌۢ ﴿20﴾

سُورَةُ الشَّمْسِ مَكِّيَّة 91
وَهِيَ سِتَّ عَشْرَةَ ءَايَة 16

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلشَّمْسِ وَضُحَىٰهَا ﴿1﴾ وَٱلْقَمَرِ إِذَا تَلَىٰهَا ﴿2﴾ وَٱلنَّهَارِ إِذَا جَلَّىٰهَا ﴿3﴾
وَٱلَّيْلِ إِذَا يَغْشَىٰهَا ﴿4﴾ وَٱلسَّمَآءِ وَمَا بَنَىٰهَا ﴿5﴾ وَٱلْأَرْضِ وَمَا طَحَىٰهَا ﴿6﴾
وَنَفْسٍ وَمَا سَوَّىٰهَا ﴿7﴾ فَأَلْهَمَهَا فُجُورَهَا وَتَقْوَىٰهَا ﴿8﴾ قَدْ أَفْلَحَ مَن زَكَّىٰهَا ﴿9﴾
وَقَدْ خَابَ مَن دَسَّىٰهَا ﴿10﴾ كَذَّبَتْ ثَمُودُ بِطَغْوَىٰهَآ ﴿11﴾ إِذِ ٱنۢبَعَثَ أَشْقَىٰهَا ﴿12﴾
فَقَالَ لَهُمْ رَسُولُ ٱللَّهِ نَاقَةَ ٱللَّهِ وَسُقْيَٰهَا ﴿13﴾ فَكَذَّبُوهُ فَعَقَرُوهَا ﴿14﴾
فَدَمْدَمَ عَلَيْهِمْ رَبُّهُم بِذَنۢبِهِمْ فَسَوَّىٰهَا ﴿15﴾ فَلَا يَخَافُ عُقْبَٰهَا ﴿16﴾

8. Shin bamu sa masa idanduna biyu banc'?.
9. Da harshe da dunbaru biyu.
10. Bamu shiryeshi hanya biyu (na hairi da sharri) bane?.
11. To meyasa bai kutsa tsauni ba?.
12. Me yasanar dakai Menene tsauni? (Girmamawa ne ga sha'anin tsaunin.)
13. Wabe wuyaye daga bauta, (wato kwance ta.)
14. Ko ciyarwa a cikin rana ma'abociyar yunwa.
15. Maraya ma'abocin zumunci a rana mai yunwa.
16. Ko miskini ma'abocin talauci madanfari da ƙasa.
17. Sannan ya kasance (zamanin kutsa tsaunin nan) yana cikin wađanda suka bada gaskiya da Allah suka wasici juna da haƙuri (kan đa'a da nesanta saɓo,) suka wasici juna da jinƙai (ga talikai.)
18. Wadancanenka (masu wađannan siffofi) sune ma'abota dama.
19. Wađanda suka kafirta da ayoyinmu sune ma'abota hauni.
20. Wuta abar kullewa (a kansu) tana kansu.

Wannan Sura Itace Suratu Shamsi

A Makka aka saukar da ita aya goma sha biyar ce (15)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba đaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan Sura ta ƙunshi Tsarkakc rai wato Babbar Aikin Sufanci a duniya da Rantsuwa a kan cewa Azaba zai afku ga masu ƙaryatawa ba makawa tamkar daya afku bisa Samudu tun dacan.)

1. Allah yayi rantsuwa da rana da hasken walaharta.
2. Da wata idan yabita, (wato ya hudo) bayan fađuwarta.
3. Da wuni idan ya baiyana rana (saboda đagawarsa.)
4. Da dare idan ya lulluɓeta (da duhunsa.)
5. Da sama da wanda ya ginata (Shine Ubangiji.)
6. Da ƙasa da wanda ya shimfiđata (Shine Ubangiji.)
7. Da kawukan đan Adam da wanda ya daidaita ta (a cikin halitta.)
8. Kuma ya kimsa mata fajircinta da tsoron Allah (jawabin rantsuwa.)
9. Haƙiƙa wanda ya tsarkaketa (daga zunubai) ya rabauta.
10. Haƙiƙa wanda ya turbuđeta (da saɓo) ya taɓe.
11. Samadu sun ƙaryata (Annabi Salihu Alaihissalamu) saboda shishshiginta.
12. Zamanin da mafi tsiyarta ya zabura (Shine ƙudaru đan Sadifu) izuwa sare taguwar (dayardarsu.)
13. Sai Manzon Allah (Annabi Salihu Alaihissalamu) yace, "ku bar taguwar Allah ta sha a ranarta," (tana da rana suna da rana.)
14/15. Suka ƙaryatashi (a cikin fađinsa wannan daga Allah take, wanda azabata sauka garesu saboda saɓa mata) suka kasheta (saboda ruwan shanta ya zama garesu,) sai Ubangijinsu ya saki gurun-gundumar azaba a kansu, (saboda zunubinsu) ya daidaita gurungundumar taɓargaza a kansu, (ba wanda ya tsira daga cikinsu.)
16. Baya tsoron mai bincikarsa.

سُورَةُ اللَّيْلِ مَكِّيَّة 92
وَهِيَ احْدَى وَعِشْرُونَ ءَايَة 21

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

* وَالَّيْلِ إِذَا يَغْشَىٰ ① وَالنَّهَارِ إِذَا تَجَلَّىٰ ② وَمَا خَلَقَ الذَّكَرَ وَالْأُنثَىٰ ③ ثمن
إِنَّ سَعْيَكُمْ لَشَتَّىٰ ④ فَأَمَّا مَنْ أَعْطَىٰ وَاتَّقَىٰ ⑤ وَصَدَّقَ بِالْحُسْنَىٰ ⑥
فَسَنُيَسِّرُهُ لِلْيُسْرَىٰ ⑦ وَأَمَّا مَنْ بَخِلَ وَاسْتَغْنَىٰ ⑧ وَكَذَّبَ بِالْحُسْنَىٰ ⑨
فَسَنُيَسِّرُهُ لِلْعُسْرَىٰ ⑩ وَمَا يُغْنِي عَنْهُ مَالُهُ إِذَا تَرَدَّىٰ ⑪ إِنَّ عَلَيْنَا
لَلْهُدَىٰ ⑫ وَإِنَّ لَنَا لَلْآخِرَةَ وَالْأُولَىٰ ⑬ فَأَنذَرْتُكُمْ نَاراً تَلَظَّىٰ ⑭
لَا يَصْلَاهَا إِلَّا الْأَشْقَى ⑮ الَّذِي كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰ ⑯ وَسَيُجَنَّبُهَا الْأَتْقَى ⑰
الَّذِي يُؤْتِي مَالَهُ يَتَزَكَّىٰ ⑱ وَمَا لِأَحَدٍ عِنْدَهُ مِن نِّعْمَةٍ تُجْزَىٰ ⑲
إِلَّا ابْتِغَاءَ وَجْهِ رَبِّهِ الْأَعْلَىٰ ⑳ وَلَسَوْفَ يَرْضَىٰ ㉑

سُورَةُ الضُّحَىٰ مَكِّيَّة 93
وَهِيَ إِحْدَى عَشْرَةَ ءَايَة 11

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

وَالضُّحَىٰ ① وَالَّيْلِ إِذَا سَجَىٰ ② مَا وَدَّعَكَ رَبُّكَ وَمَا قَلَىٰ ③

Wannan Sura Itace Suratul Laili

a Makka aka saukar da ita aya ishirin da ɗayace (21)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Ubangiji ya rantse da cewa mutane masu saɓawane cikin aiyukansu da sakamakonta, sannan ya bada tsoro da wuta ga wanda ya saɓeshi da haramcin wuta ga wanda yabishi. Ta saukane ga Saiyidina Abubakar Allah ya ƙara masa yarda amin.)

1. Allah ya rantse da darc idan ya lulluɓe (dukan abinda yake sama da ƙasa da duhunsa.)
2. Ya rantse da wuni idan ya yaye.
3. Ya rantse da wanda ya halicci na miji da mace (Annabi Adamu da Hauwa'u.)
4. Haƙiƙa aikinku dabam-dabamne, wani aikin Aljanna yakeyi da ɗa'a, wani aikin Wuta yake yi da saɓo)
5. Amma wanda ya bada (haƙƙin Allah) yaji tsoron Allah.
6. Ya gasgatada husna (Itace LA ILAHA ILLALLAHU.)
7. To da sannu zamu shiryeshi don aikin Aljanna.
8. Amma wanda yayi rowa (da haƙƙin Allah) ya wadata (ga buran sakamakonsa don girman kai.)
9. Ya ƙaryatada - LA ILAHA ILLALLAHU -
10. Da sannu zamu shirye shi, izuwa mafi tsanani Itace wuta.
11. Dukiyarsa bazata wadatar dashi komai ba idan yagangara (a cikin wuta.)
12. Haƙiƙa baiyana hanyar shiriya daga hanyar ɓata, yana garemu, don a rungumi hanyar shiriya a nisanci hanyar ɓata).
13. Haƙiƙa lahira da duniya tamuce, (wanda ya neme su daga waninsu yayi kuskure.)
14. To na tsoratar daku ,wuta da take zaɓaɓɓaka.
15. Ba mai shigarta sai shaƙiyi.
16. Wanda ya ƙaryata Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) ya bada baya (ga buran imani.)
17. Da sannu za a nisantar da mai tsoron Allah ga buranta.
18. (Halin kasancewarsa,) wanda yake fitar da dukiyarsa donya tsarkaka) gurin Allah badon riya ba badon aji ba, saiya zama tsarkakakke gurin Allah, wannan aya ta sauka ne a cikin Saiyidina Abubakar Allah ya ƙara masa yarda, zamanin daya sayi Bilalu, wanda ake masa azaba bisa imaninsa ya 'yantashi sai kafirai sukace, "af yayi wancanenkane saboda wani alheri daya afku tsakaninsu, sai Allah ya saukar da...).
19. Ba wani mutum da yake da ni'ima da ake sakata ga Abubakar (allah ya ƙara yarda gareshi.)
20. Saidai ya aikata haka don yardar Zatin Ubangijinsa mafi ɗaukaka.
21. Lallai da sannu zai yarda da sakamako da abindaza a bashi na Aljanna. (Ita wannan aya ta gama da wanda ya kwatanta misalin wannan aiki nasa Raliyallahu anhu, za a nesantashi daga wuta, za a bashi sakamako.)

Wannan Sura Itace Suratu Duha

a Makka aka saukar da ita aya goma sha ɗayace (11)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Allah yayi rantsuwa a cikin Wadduhe da cewa Bai bar Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallama ba, baiƙi shiba, da kuma cewa ƙarshensa yafi farkonsa, kuma cewa zai bashi harya yarda dashi, sannan za a nemi iƙrari dashi ga ba'alin darajoji. Yayin data sauka Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama sai yayi Kabbara, saboda haka aka Sunnantayin Kabbara yayinsa Shine ALLAHU AKBAR, ko LA ILAHA ILLALLAHU ALLAHU AKBAR a ƙarshenta da ƙarshen kowace sura bayanta.)

1. Ubangiji ya rantse da farkon wuni ko dukkansa.
2. Ya rantse da darc idan ya lulluɓe (da duhunsa.)
3. Ubangijinka bai barka ba baiƙi ka ba. (Wannan ya sauka ne yayin jinkirin saukar wahayi ga buransa kwana goma sha biyar (15) sai sukace Ubangijinsa yabar shi kuma yaƙishi.)

وَلَلْأٓخِرَةُ خَيْرٌ لَّكَ مِنَ الْأُولَىٰ ﴿4﴾ وَلَسَوْفَ يُعْطِيكَ رَبُّكَ فَتَرْضَىٰ ﴿5﴾
أَلَمْ يَجِدْكَ يَتِيمًا فَـَٔاوَىٰ ﴿6﴾ وَوَجَدَكَ ضَآلًّا فَهَدَىٰ ﴿7﴾
وَوَجَدَكَ عَآئِلًا فَأَغْنَىٰ ﴿8﴾ فَأَمَّا الْيَتِيمَ فَلَا تَقْهَرْ ﴿9﴾
وَأَمَّا السَّآئِلَ فَلَا تَنْهَرْ ﴿10﴾ وَأَمَّا بِنِعْمَةِ رَبِّكَ فَحَدِّثْ ﴿11﴾

سُورَةُ الشَّرْحِ مَكِّيَّةٌ 94
وَهِيَ ثَمَانِي ءَايَاتٍ 8

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

* أَلَمْ نَشْرَحْ لَكَ صَدْرَكَ ﴿1﴾ وَوَضَعْنَا عَنكَ وِزْرَكَ ﴿2﴾ الَّذِيٓ
أَنقَضَ ظَهْرَكَ ﴿3﴾ وَرَفَعْنَا لَكَ ذِكْرَكَ ﴿4﴾ فَإِنَّ مَعَ الْعُسْرِ يُسْرًا ﴿5﴾
إِنَّ مَعَ الْعُسْرِ يُسْرًا ﴿6﴾ فَإِذَا فَرَغْتَ فَانصَبْ ﴿7﴾ وَإِلَىٰ رَبِّكَ فَارْغَب ﴿8﴾

سُورَةُ التِّينِ مَكِّيَّةٌ 95
وَهِيَ ثَمَانِي ءَايَاتٍ 8

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

وَالتِّينِ وَالزَّيْتُونِ ﴿1﴾ وَطُورِ سِينِينَ ﴿2﴾ وَهَٰذَا الْبَلَدِ الْأَمِينِ ﴿3﴾
لَقَدْ خَلَقْنَا الْإِنسَانَ فِيٓ أَحْسَنِ تَقْوِيمٍ ﴿4﴾ ثُمَّ رَدَدْنَٰهُ أَسْفَلَ سَٰفِلِينَ ﴿5﴾

ربع

4. Kuma lallai lahira tafi maka daga duniya (domin abinda yake gareka a cikinta na daga karamomi a aljanna.)
5. Da sannu Ubangijinka zai baka (kyauta gwaggwaba maɗaukakiya) sai ka yarda (da ita, Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama yace "In ko hakane ni bazan yarda ɗaya daga cikin al'ummata a cikin wuta ba.")
6. Shin bai sameka kana maraya bane ya tattaraka (ga Abu ɗalib da rashin mahaifinka tun gaban haihuwarka?)
7. Bai sameka kana mai nema ga Ubangiji ba? (Mai dimuwa ga buran abinda kake kai a yanzu na shari'a) ya shiryeka (izuwa gareta ya shiryeka ga yardarsa da shari'arsa, ya shiryeka izuwa gareshi izuwa' arziki.)
8. Ya sameka mabuƙaci ya wadata (ka da abinda ya baka na ganima da waninta.)
9. Amma maraya kada kayi masa rinjaye (da karɓar dukiyarsa.)
10. Amma mai tambaya (saboda talaucinsa) kada kayi masa tsawa.
11. Amma da ni'imar Ubangijinka (da Annabci) to daidaita.

Wannan sura Itace Suratul Sharhi

A Makka aka saukar da ita aya takwas ce (8)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan sura tana ƙidaya Ni'imomin da Allah yayi a bisa Annabinsa Sallallahu alaihi wasallama da kwaɗaitar dashi kan aiki).

1. Shin bamu buɗe ƙirjinka bane donka (da Annabci da waninsa kamar ganawa da Allah da kiran mutane izuwa Allah?)
2. Bamu saryar da nauyin ka bane ga buranka?
3. Wanda ya nauyaya bayanka.
4. Bamu ɗaukaka ambaton ka bane donka, (Shine a ambace ka tareda ambatona a kiran salla da iƙama da tahiya da huɗ ubada waninta.
5. Haƙiƙa sauƙi yana tareda tsanani.
6. Haƙiƙa sauƙi yana tareda tsanani, (Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama yayi gogaiya da tsanani da kafirai, sannan sauƙi ya tabbata gareshi.)

(KARATUN WURUDAI DA ZIKIRI BAYAN SALLOLI)

7. Idan ka gama daga salla sai ka kafu (kayi ta addu'a.)
8. Ka ƙanƙan dakai izuwa Ubangijinka.

Wannan Sura Itace Suratu Tini

A Makka aka saukar da ita aya takwas ce (8)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Ubangiji ya rantse cikinta cewa ya halicci muturri ya daidai tashi sannan ya mai dashi ƙasan ƙasa, sai Muminai, tosu suna da lada mai girma.)

1. Ubangiji ya rantse da Baure da zaituni.
2. Da dautsen ɗuri Sina (wanda Allah yayi zance da Annabi Musa Alaihissalamu a kansa, ma'anar Sinina wanda akayi masa albarka da kyawawan itatuwa masu 'ya'ya.)
3. Da wannan gari amintacce (Shine Makka saboda mutane sun amince cikinsa na jahiliyya da zamanin Musulunci.)
4. Haƙiƙa mun halicci jinsin mutum a mafi kyan daidaitawa da surarsa.
5. Sannan muka mai dashi mafi ƙasan ƙasa (a cikin ba'alin daidaiwarsa, yana nufin tsufa ne da rauni.

إِلَّا الَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ الصَّٰلِحَٰتِ فَلَهُمُۥٓ أَجْرٌ غَيْرُ مَمْنُونٍ ۝6
فَمَا يُكَذِّبُكَ بَعْدُ بِالدِّينِ ۝7 أَلَيْسَ اللَّهُ بِأَحْكَمِ الْحَٰكِمِينَ ۝8

96 سُورَةُ الْعَلَقِ مَكِّيَّةٌ
وَهِيَ عِشْرُونَ ءَايَةً 20

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

اِقْرَأْ بِاسْمِ رَبِّكَ الَّذِي خَلَقَ ۝1 خَلَقَ الْإِنسَٰنَ
مِنْ عَلَقٍ ۝2 اِقْرَأْ وَرَبُّكَ الْأَكْرَمُ ۝3 الَّذِي عَلَّمَ بِالْقَلَمِ ۝4
عَلَّمَ الْإِنسَٰنَ مَا لَمْ يَعْلَمْ ۝5 كَلَّا إِنَّ الْإِنسَٰنَ لَيَطْغَىٰٓ ۝6
أَن رَّءَاهُ اسْتَغْنَىٰٓ ۝7 إِنَّ إِلَىٰ رَبِّكَ الرُّجْعَىٰٓ ۝8
أَرَأَيْتَ الَّذِي يَنْهَىٰ ۝9 عَبْدًا إِذَا صَلَّىٰٓ ۝10
أَرَأَيْتَ إِن كَانَ عَلَى الْهُدَىٰٓ ۝11 أَوْ أَمَرَ بِالتَّقْوَىٰٓ ۝12
أَرَأَيْتَ إِن كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰٓ ۝13 أَلَمْ يَعْلَم بِأَنَّ اللَّهَ
يَرَىٰ ۝14 كَلَّا لَئِن لَّمْ يَنتَهِ ۝15 لَنَسْفَعًا بِالنَّاصِيَةِ ۝16
نَاصِيَةٍ كَٰذِبَةٍ خَاطِئَةٍ ۝17 فَلْيَدْعُ نَادِيَهُۥ ۝18 سَنَدْعُ
الزَّبَانِيَةَ ۝19 كَلَّا لَا تُطِعْهُ وَاسْجُدْ وَاقْتَرِبْ ۝20

6. Saidai waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargaru to suna da lada ba abin yankewa ba. (A cikin Hadisi idan Mumini ya isa na daga tsufa ga buran aiki sai a rubuta masa abinda ya kasance yana aikatawa.)
7. Menene ya sa ka ƙaryata, bayan abinda aka ambata na daga halittar mutum kai kafiri?
8. Shin Ubangiji bashine mafi iya mahukunta zartar da hukunci bane? (Shine, BALE WANAHANU ALA ZALIKA MINASH-SHAHIDIN).

Wannan Sura Itace Suratul ALAƘI

a Makka aka saukar da ita aya ishirin ce (20)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniyagaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(A cikin wannan sura akwai umarnin Annabi Sallallahu alaihi wasallama da karatu da mabaiyanar ikon Allah tareda mutum da bayanin ba'alin sifofinsa.) Farkon wannan aya izuwa MAL-AM YA ALAM, Shine farkon abinda ya fara sauka na Alƙur'ani. Wancanenka kuwa a Kogon Hira ne Buhari ya ruwaito shi.

1. Ka karanta da sunan Ubangijinka wanda ya halicci (talikai.)
2. Ya halicci mutum daga gudan jini.
3. Yi karatu, Ubangijinka ne mafi karamci, (wanda wani karimi bazai kwatance shi ba.)
4. Wanda yasanar da rubutu da alƙalami, (farkon wanda yayi rubutu da alƙalami Annabi Idrisu Alaihissalamu.)
5. Yasanar da mutum abinda bai sani ba (na shiriya da rubutu da sana'a da waninta.)
6. Lallai mutum haƙiƙa yana shishshigi.
7. Don yaga ya wadata da dukiya, (ya sauka cikin Abi Jahil.)
8. Haƙiƙa koruwa izuwa Ubangijinka ne.
9. Bamu labarin wanda yake hana.
10. Bawa idan yayi salla [1]
11. Bamu labarin in wanda aka hana ɗin ya kasance kan shiriya.
12. Ko yayi umarni da aikin shiriya (Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama.)
13. Bani labari in mai hana Annabi (Sallallahu alaihi wa sallama) ya karyata, ya bada bayaga bu-ran imani.
14. Shin bai sani bane cewa Allah yana ganinsa bane?
15. Hir! Wallahi idan bai hanu ga buran abinda yake kansa na ka-firci ba.
16. Lallai zamuyi danda da makwarkwaɗarsa (izuwa wuta.)
17. Makwarkwaɗa maƙaryaciya mai kuskure.
18. Ya kirawo mutanen mazaunin nasa ('yan dandalinsa da can yace da Ma'aikin Allah Sallallahu alaihi wasallama a sanda yayi masa tsawa ga buran salla, yace ai lallai ka sani a Makka babu mafi yawan 'yan dandali daga gareni. Wallahi zan cika wannan zaza in naga dama, da dawakai masu silai silai da samari marasa gemu.)
19. Da sannu zamu kirawo Zabaniyawa (Mala'ikune kaurara, saboda halakar dashi a cikin Hadisi daya kirawo 'yan dandalinsa ɗin da Zabaniyawa [2] sun fizge shi ƙarara.)
20. Hir! Kadaka daka tasa (a cikin barin salla,) kayi salla don Allah ka kusance shi da ɗa'a.)

1) mai hamin shine Abu jahil wanda aka hane shine Manzon Allah. - sanajiy -
2) Sune Malaikun jahannama Kamar Sojoji anan duniya. - Sanajiy

97 سُورَةُ الْقَدْرِ مَكِّيَّة
وَهِيَ خَمْسُ ءَايَاتٍ 5

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

ثمن
* إِنَّا أَنزَلْنَاهُ فِي لَيْلَةِ الْقَدْرِ ﴿1﴾ وَمَا أَدْرَاكَ مَا لَيْلَةُ الْقَدْرِ ﴿2﴾
لَيْلَةُ الْقَدْرِ خَيْرٌ مِّنْ أَلْفِ شَهْرٍ ﴿3﴾ تَنَزَّلُ الْمَلَائِكَةُ وَالرُّوحُ
فِيهَا بِإِذْنِ رَبِّهِم مِّن كُلِّ أَمْرٍ ﴿4﴾ سَلَامٌ هِيَ حَتَّىٰ مَطْلَعِ الْفَجْرِ ﴿5﴾

98 سُورَةُ الْبَيِّنَةِ مَدَنِيَّة
وَهِيَ ثَمَانِي ءَايَاتٍ 8

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

لَمْ يَكُنِ الَّذِينَ كَفَرُوا مِنْ أَهْلِ الْكِتَابِ وَالْمُشْرِكِينَ مُنفَكِّينَ حَتَّىٰ تَأْتِيَهُمُ
الْبَيِّنَةُ ﴿1﴾ رَسُولٌ مِّنَ اللَّهِ يَتْلُو صُحُفًا مُّطَهَّرَةً ﴿2﴾ فِيهَا كُتُبٌ قَيِّمَةٌ ﴿3﴾ وَمَا تَفَرَّقَ
الَّذِينَ أُوتُوا الْكِتَابَ إِلَّا مِن بَعْدِ مَا جَاءَتْهُمُ الْبَيِّنَةُ ﴿4﴾ وَمَا أُمِرُوا إِلَّا لِيَعْبُدُوا
اللَّهَ مُخْلِصِينَ لَهُ الدِّينَ حُنَفَاءَ وَيُقِيمُوا الصَّلَاةَ وَيُؤْتُوا الزَّكَاةَ وَذَٰلِكَ دِينُ
الْقَيِّمَةِ ﴿5﴾ إِنَّ الَّذِينَ كَفَرُوا مِنْ أَهْلِ الْكِتَابِ وَالْمُشْرِكِينَ فِي نَارِ جَهَنَّمَ خَالِدِينَ فِيهَا أُولَٰئِكَ
هُمْ شَرُّ الْبَرِيَّةِ ﴿6﴾ إِنَّ الَّذِينَ ءَامَنُوا وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ أُولَٰئِكَ هُمْ خَيْرُ الْبَرِيَّةِ ﴿7﴾

Wannan Sura Itace Suratul Ƙadari

a Makka aka saukar da ita aya biyar ce (5)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan sura tayi zance da farkon saukar Alƙur'ani kuma cewa shiya sauka a daren Lailatul ƙadri).

1. Haƙiƙa mu mun saukar da Alƙur'ani jumla (wato a mulmule, daga Lauhul mahtuzu izuwa saman duniya) a daren Alƙadari (wato girma da ɗaukaka.)
2. Wane abu ne yasanar dakai (Ya Muhammadu Sallallahu alaihi wasallama Menene daren alƙadari? don girman Alƙawaru da da Manakanfanwar fa).
3. Daren Alƙadari yafi wata dubu (wecce babu daren Alƙadari a cikinta, aiki na gari a cikinta yafi aiki a dare dubu wanda ba a cikinta ba.)
4. Mala'iku suna sauka da Mala'ika Jibrilu a daren, da izinin Ubangijinsu (wato da umarninsa, saboda kowane al'amari da Allah ya hukun tashi a cikinta tun daga wannan daren har izuwa shekara mai zuwa.)
5. Ita daren Alƙadari ita gaisuwa ce (daga Mala'iku izuwa Muminai, bazasu wuce ga Mumini ko Mumina ba, face sai sun sallama gareshi har hudowar alfijir.)

Wannan Sura Itace Suratul Baiyinati

A Madina aka saukar da ita aya takawas ce (8)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Akwai Raddi a kan kafirai na mushurkai da Ahlul Kitabi da bayanin cewa abinda Annabi Sallallahu alaihi wasallama yazo daShine gaskiya sannan ambaton sakamakon wanda ya wanzu kan kafirci daga cikinsu da wandaya bada gaskiya da Manzon Allah Sallallahu alaihi wa salla-ma.)

1. Waɗanda suka kafirta sune Ah-lul Kitabi da mushirkai, (masu bautar gumaka) basu kasance masu kawa daga abinda suke kai ba har saida hujja mabaiyaniya tazo musu (Itace Annabi Sallallahu alaihi wasallama.)
2. Manzo daga Allah (Annabi Sallallahu alaihi wasallama) yana karanta littattafai ababan tsarkakewa (ga buran ɓarna.)
3. Akwai hukunce-hukunce abar rubutawa a cikinta madaidaiciya (yana karantawar abinda wannan ya ƙunsa Shine Alƙur'ani, akwai daga garesu wanda ya bada gaskiya dashi da wanda ya kafirta.)
4. Waɗanda ka baiwa littafi basuyi dabab-daban ba (a cikin imani dashi Sallallahu alaihi wasallama) sai bayan Annabi (Sallallahu alaihi wasallama) yazo musu (da Alƙur'ani wanda yazo dashi don mu'ujuza gareshi, gaban zuwansa sun kasance a hade da imani dashi in yazo, sai waɗanda suka kafirta dashi daga cikinsu sukayi masa hassada.)
5. Ba a umarcesu (cikin littafinsu Attaura da Injila ba,) sai donsu bautwa Allah suna masu tsarkakewar bauta daga shirka a gareshi, masu tabbata kan totar (kan addinin Annabi Ibrahimu Alaihissalamu da Annabi SallAllahu alahihi wasallama kuma su tsaida salla (wato su kyautata,) su bada zakka, wancanenka Shine tafarki madaidaici.
6. Haƙiƙa waɗanda suka kafirta sune mazowa littafi da mushrikai suna cikin wutar jahannama masu dawwama a cikinta, waɗancanenka sune sharrin talikai.
7. Waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiki nagargru waɗancanenka sune fiyayyun talikai.

جَزَآؤُهُمْ عِندَ رَبِّهِمْ جَنَّٰتُ عَدْنٍ تَجْرِي مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا
أَبَدًا رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُوا عَنْهُ ذَٰلِكَ لِمَنْ خَشِيَ رَبَّهُ ﴿8﴾

سورة الزلزلة مدنية 99
وهي ثماني آيات 8

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِذَا زُلْزِلَتِ ٱلْأَرْضُ زِلْزَالَهَا ﴿1﴾ وَأَخْرَجَتِ ٱلْأَرْضُ أَثْقَالَهَا ﴿2﴾
وَقَالَ ٱلْإِنسَٰنُ مَا لَهَا ﴿3﴾ يَوْمَئِذٍ تُحَدِّثُ أَخْبَارَهَا ﴿4﴾ بِأَنَّ رَبَّكَ
أَوْحَىٰ لَهَا ﴿5﴾ يَوْمَئِذٍ يَصْدُرُ ٱلنَّاسُ أَشْتَاتًا لِّيُرَوْا أَعْمَٰلَهُمْ ﴿6﴾
فَمَن يَعْمَلْ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ خَيْرًا يَرَهُ ﴿7﴾ وَمَن يَعْمَلْ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ شَرًّا يَرَهُ ﴿8﴾

سورة العاديات مكية 100
وهي إحدى عشرة آية 11

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلْعَٰدِيَٰتِ ضَبْحًا ﴿1﴾ فَٱلْمُورِيَٰتِ قَدْحًا ﴿2﴾ فَٱلْمُغِيرَٰتِ صُبْحًا ﴿3﴾
فَأَثَرْنَ بِهِ نَقْعًا ﴿4﴾ فَوَسَطْنَ بِهِ جَمْعًا ﴿5﴾ إِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ لِرَبِّهِ
لَكَنُودٌ ﴿6﴾ وَإِنَّهُ عَلَىٰ ذَٰلِكَ لَشَهِيدٌ ﴿7﴾ وَإِنَّهُ لِحُبِّ ٱلْخَيْرِ لَشَدِيدٌ ﴿8﴾

8. Sakamakonsu nan ga Ubangijinsu aljannatai na zama, ƙoramu suna gudana a cikinta, madauwama a cikinta, Allah ya yarda garesu su kuma sun yarda gareshi (da sakamakonsu,) wancanenka ga wanda yaji tsoron Ubangijinsa (ya hanu ga buran saɓon Ubangiji.)

Wannan Sura Itace Suratu Zalzalati
a Makka aka saukar da ita aya tara ce (9)
Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Ubangiji ya tabbatar a cikinta cewa kowane Alheri Allah zaiyi sakamako a cikinsa shi kuma sharri komai ƙanƙantarsa za a sakawa mai shi a kansa, amma a Ranar Alƙiyama.)

1. Idan aka girgiza ƙasa (ranar Alƙiyama) irin girgizawar daya dace da ita.
2. ƙasa ta fitar da taskokinta (da matattunta ta fitar dasu a kan bayanta.)
3. Mai kafircewa da tashin Alƙiyama yace "me ya sameta."
4. A wannan lokaci ne zata zantar da labaran ta (na hairi ko sharri.)
5. Saboda cewa Ubangijinka ya aiko gareta (da wancanenka, a cikin hadisi za tayi shaida a kan kowane bawa ko kuyanga da abinda ya aikata a kanta.)
6. A wannan rana mutane suke juyawa (daga gurin hisabi) daban daban (wani izuwa dama izuwa Aljanna, wani izuwa hagun izuwa wuta.)
7. Don a nuna musu sakamakonsu (na alheri izuwa Aljanna ko wuta.)
8. Wanda ya aikata misalin ƙwayar kiyashi na alheri zaiga sakamakonsa.
9. Wanda ya aikata misalin ƙwayar kiyashi na sharri zai ga sakamakonsa.

Wannan Sura Itace Suratu Adiyati
A Makka aka saukar da ita aya goma sha ɗayace (11)
Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(A cikin wannan Surar Ubangiji yana rantsuwa mutum wanda Allah yayi ni'ima a gareshi mai butulci ne sannan ya bashi tsoro da uƙuba mai tsanani ranar Alƙiyama. Kuma cewa Ubangiji mai shaidane a kan wannan da cewa wannan kafirin mutum mai son dukiya ne marowaci ne.)

1. Ubangiji ya rantse da dawakai waɗanda suke gudu a yaƙi, idan cikinta yana ƙara ƙarar tana ɗan ƙanƙanen sauti daga cikinta.
2. Sannan ya rantse da masu tashin wuta da ƙofatanta tashi, (in tai tafiya kan duwarwatsu da daddare.)
3. Ubangiji ya rantse da dawakai masu kai hari lokacin asuba.
4. Su turnuƙa ƙura turnuƙawa a gurin gudun nasu.
5. Suka kutsa cikin ƙurar nan baki ɗaya.
6. Haƙiƙa mutum kafiri mai butulcewane ga Ubaangijinsa.
7. Lallai mai shaidarwa ne da kansa da wannan aiki.
8. Haƙiƙa shi mai tsananine da son alheri (wato dukiya, kuma yana rowa dashi.)

1) Wato Annabawa, da waliyyai da Salihai. - Sa-najiy -

ربع

* أَفَلَا يَعۡلَمُ إِذَا بُعۡثِرَ مَا فِي ٱلۡقُبُورِ ۝9 وَحُصِّلَ
مَا فِي ٱلصُّدُورِ ۝10 إِنَّ رَبَّهُم بِهِمۡ يَوۡمَئِذٖ لَّخَبِيرُۢ ۝11

سورة القارعة مكية 101
وهي عشر آيات 10

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلۡقَارِعَةُ ۝1 مَا ٱلۡقَارِعَةُ ۝2 وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡقَارِعَةُ ۝3 يَوۡمَ يَكُونُ
ٱلنَّاسُ كَٱلۡفَرَاشِ ٱلۡمَبۡثُوثِ ۝4 وَتَكُونُ ٱلۡجِبَالُ كَٱلۡعِهۡنِ ٱلۡمَنفُوشِ ۝5
فَأَمَّا مَن ثَقُلَتۡ مَوَٰزِينُهُۥ ۝6 فَهُوَ فِي عِيشَةٖ رَّاضِيَةٖ ۝7 وَأَمَّا مَنۡ خَفَّتۡ
مَوَٰزِينُهُۥ ۝8 فَأُمُّهُۥ هَاوِيَةٞ ۝9 وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا هِيَهۡ ۝10 نَارٌ حَامِيَةُۢ ۝11

سورة التكاثر مكية 102
وهي ثماني آيات 8

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

أَلۡهَىٰكُمُ ٱلتَّكَاثُرُ ۝1 حَتَّىٰ زُرۡتُمُ ٱلۡمَقَابِرَ ۝2 كَلَّا سَوۡفَ تَعۡلَمُونَ ۝3
ثُمَّ كَلَّا سَوۡفَ تَعۡلَمُونَ ۝4 كَلَّا لَوۡ تَعۡلَمُونَ عِلۡمَ ٱلۡيَقِينِ ۝5 لَتَرَوُنَّ ٱلۡجَحِيمَ ۝6
ثُمَّ لَتَرَوُنَّهَا عَيۡنَ ٱلۡيَقِينِ ۝7 ثُمَّ لَتُسۡـَٔلُنَّ يَوۡمَئِذٍ عَنِ ٱلنَّعِيمِ ۝8

9. Shin bai sani bane idan aka fitar da matattu dasuke cikin kaburbura?
10. Aka faiyacc abinda yake cikin ƙiraza (na kafirci da imani.)
11. Haƙiƙa Ubangijinsu lallai masaninc dasu a wannan rana (zai saka musu kan kafircinsu.)

Wannan Sura Itace Suratul Ƙari'a

A Makka aka saukar da ita aya goma ce (10)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(AKWAI BA'ALIN ABABAN KALLO RANAR ALƘIYAMA)

1. Ma ƙwarƙwashiya, (Alƙiyama kenan da take ƙwarƙwasan zukata da tsarmakatanta.) Menene maƙwarƙwashiya? (Ban tsoronc daga sha'aninta.)
2. Wane abune yasanar dakai Menene maƙwarƙwashiya?
3. Ranar da mutane suka zama kamar fari madaidaita ba'alinsu yana shiga cikin ba'ali saboda ɗimuwa har ayi kira izuwa sakamako.)
4. Duwarwatsu su zama kamar angalara abar kaɗewa da tsirkiyar baka har tayi daidai tareda ƙasa.
5. Amma wanda ma'aunansa sukayi nauyi (Shine kyawawan aiyukansa sukayi rinjaye a kan miyagu.)
6. To shi yana cikin rayuwa data yarda dashiya yarda da ita.
7. Amma wanda sukayi sauƙi sukayi shafal; (saiyi'o'insa tayi rinjaye a kan hasanoninsa.)
8. To mazauninsa Hawiya.
9. Wane abu ne yasanar dakai Menene Hawuya?
10. Ita wutace mai tsananin zafi.

Wannan Sura Itace Suratul Takasuru

A Makka aka saukar da ita aya takwas ce (8)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(A cikin wannan Sura Ubangiji yana tsoratar damu yawan tara kuɗi da alfarma da 'ya'ya ye yana ƙarfafa cewa lallai azabar masu saɓo saita afku kuma Jahannama gaskiyace kuma za a tam-bayemu ga ni'imomin da mukaji aduniya.)

1. In alfahari da dukiya da 'ya'yaye da alfarma ya shagalar daku ,ga buran tanajin lahira.
2. Har kuka mutu akabinne ku a cikin kaburbura.
3. Hir! da sannu zakusan (aƙibar al'amarinku.)
4. Sannan hir! da sannu zaku san (aƙibar al'amarin yayin fitar rai.)
5. Dahir da kuna da sani. Sanin yaƙini (na ƙarshen al'amarinku bada zu ku shagala da fariyaga buran tanadin lahira ba.)
6. Wallahi da sannu zaku ga wutar Jahannama.
7. Sannan Wallahi zaku ganta gani na idon yaƙini (bana sanin yaƙini ba.)
8. Sannan Wallahi a rannan za a tambayeku ga ni'imomi (daya ni'imta muku a duniya kamar lafiyar jiki da samun dama da zaman lafiya cikin rashin tsoro da abinci mai daɗi da ruwa mai sanyi da sauransu.)

103 سُورَةُ العَصرِ مَكِّيَّة
وَهِيَ ثَلَاثُ ءَايَاتٍ 3

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلْعَصْرِ ① إِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ لَفِى خُسْرٍ ② إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟
وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَتَوَاصَوْا۟ بِٱلْحَقِّ وَتَوَاصَوْا۟ بِٱلصَّبْرِ ③

104 سُورَةُ الهُمَزَةِ مَكِّيَّة
وَهِيَ تِسْعُ ءَايَاتٍ 9

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَيْلٌ لِّكُلِّ هُمَزَةٍ لُّمَزَةٍ ① ٱلَّذِى جَمَعَ مَالًا وَعَدَّدَهُۥ ② يَحْسَبُ أَنَّ مَالَهُۥٓ أَخْلَدَهُۥ ③
كَلَّا لَيُنۢبَذَنَّ فِى ٱلْحُطَمَةِ ④ وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا ٱلْحُطَمَةُ ⑤ نَارُ ٱللَّهِ ٱلْمُوقَدَةُ ⑥
ٱلَّتِى تَطَّلِعُ عَلَى ٱلْأَفْـِٔدَةِ ⑦ إِنَّهَا عَلَيْهِم مُّؤْصَدَةٌ ⑧ فِى عَمَدٍ مُّمَدَّدَةٍۭ ⑨

105 سُورَةُ الفِيلِ مَكِّيَّة
وَهِيَ خَمْسُ ءَايَاتٍ 5

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ثمن

* أَلَمْ تَرَ كَيْفَ فَعَلَ رَبُّكَ بِأَصْحَٰبِ ٱلْفِيلِ ① أَلَمْ يَجْعَلْ كَيْدَهُمْ فِى تَضْلِيلٍ ②

Wannan Itace Suratul Asri

A Makka aka saukar da ita aya uku ce (3)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Ubangiji ya rantse cewa mutum yana cikin taɓewa sai wanda Allah ya kiyayeshi, sai Muminai waɗanda sukayi aiki da ilimi.)

1. Ubangiji ya rantse da la'asar, (zamani dukkansa ko sallar la'asar,) haƙiƙa dukkan mutum yana cikin taɓewa (a cikin cinikinsa).
2. Sai waɗanda suka bada gaskiya sukayi aiyukka nagargaru (waɗannan basa Cikin taɓewa.)
3. Sukayi wasiceceniya da imani, sukayi wasiceceniya (a kan ɗa'a) da haƙuri (ga bala'i da dauriya akan ɗa'a da dauriya ga buran saɓo.)

Wannan Sura Itace Suratul Humazad

A Makka aka saukar da ita aya tara ce (9)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Akwai laifintawa ga Annamini a cikinta da Alƙawari gareshi dashiga wuta abar kifawa a kansa ɗaga kowace nahiya.)

1. Azabar Jahanma ta tabbata ga *dukkan m*ai yawan giba(Shine kama suna wato raɗa) da cin fuska na jama'a, (ta sauka a cikin wanda yake raɗa ga Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama da Muminai kamar Umaiyatu ibn Khalafin da Walidu ɗan Mugira da waninsa.)
2. Wanda ya tattara dukiyaya ƙirgeta (ya ƙiƙƙirgata ya tanadeta saboda musifun zamani.)
3. Yana zaton dukiyarsa zata mai dashi madauwami (bazai mutu ba.)
4. Hir! daga wannan aiki, Wallahi za a jefa shi a cikin Huɗama, (wutar da take karairaya dukkan abinda akajefa cikinta.)
5. Me yasanar dakai meye Huɗama? (saboda girman sha'aninta.)
6. Itace wutar Allah abar hurawa.
7. Wacce take tsinKaye kan zukata (ta ƙoncta, raɗaɗinta yafi zafi daga raɗaɗin wutarta, saboda taushin zuciya yafi taushin Jiki.)
8. Ita wutar abar kifawa ce a kansu (ta kewaye dasu ta kowace nahiya.)
9. A cikin al'amudai ababan miƙawa, (wacce ba hijabi tsakaninsu da wutar, Allah ya kiyashemu, Allah ya kiyashemu Amin.)

Wannan Sura Itace Suratul Fili

A Makka aka saukar da ita aya biyar ce (5)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(AKWAI ƘISSAR AS-HABUL FILI A CIKINTA)

1. Yi mana kishin baka ganiba yadda Ubangijinka ya aikata ga ma'abota giwa, (shi giwan ana kiransa Mahmudu, Ashabil Fili kuwa Abrahatu Sarkin Yemen da sojojinsa, ya gina kansa a san'a'a donya juyar da Alhazai ga buran Makkah izuwa gareta, sai wani mutum Bakinane yayi najasa ya shafe alƙiblarta da gayaɗin don wulaƙantawa gareta ita kanisar. Saboda haka Ab-rahatu ya rantse zai rushe Ka'aba, yazo Makka da sojojinsa a kan giwawaye wanda Mahmudu yake kan gabansu a yayin da suka fuskanto Makka da sojojinsa sai Ubangiji ya labarta abinda ya faɗa.)
2. Shin Ubangiji bai sanya kaidinsu (na-rushe Ka'aba) a cikin taɓewa ba?
3. Ya aiko musu da tsuntsaye bun-dubundu (wato ƙungiya-ƙungiya.)

وَأَرْسَلَ عَلَيْهِمْ طَيْرًا أَبَابِيلَ ③ تَرْمِيهِم بِحِجَارَةٍ مِّن سِجِّيلٍ ④ فَجَعَلَهُمْ كَعَصْفٍ مَّأْكُولٍ ⑤

سُورَةُ قُرَيْشٍ مَكِّيَّةٌ 106
وَهِيَ خَمْسُ ءَايَاتٍ 5

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

لِإِيلَافِ قُرَيْشٍ ① إِيلَافِهِمْ رِحْلَةَ الشِّتَاءِ وَالصَّيْفِ ② فَلْيَعْبُدُوا
رَبَّ هَٰذَا الْبَيْتِ ③ الَّذِي أَطْعَمَهُم مِّن جُوعٍ ④ وَءَامَنَهُم مِّنْ خَوْفٍ ⑤

سُورَةُ الْمَاعُونَ مَكِّيَّةٌ 107
وَهِيَ سِتُّ ءَايَاتٍ 6

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

أَرَأَيْتَ الَّذِي يُكَذِّبُ بِالدِّينِ ① فَذَٰلِكَ الَّذِي يَدُعُّ الْيَتِيمَ ② وَلَا يَحُضُّ عَلَىٰ طَعَامِ الْمِسْكِينِ ③
فَوَيْلٌ لِّلْمُصَلِّينَ ④ الَّذِينَ هُمْ عَن صَلَاتِهِمْ سَاهُونَ ⑤ الَّذِينَ هُمْ يُرَاءُونَ وَيَمْنَعُونَ الْمَاعُونَ ⑥

سُورَةُ الْكَوْثَرِ مَكِّيَّةٌ 108
وَهِيَ ثَلَاثُ ءَايَاتٍ 3

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

إِنَّا أَعْطَيْنَاكَ الْكَوْثَرَ ① فَصَلِّ لِرَبِّكَ وَانْحَرْ ② إِنَّ شَانِئَكَ هُوَ الْأَبْتَرُ ③

4. Tana jifansu da tsakwakwani na Sijjin (kwayukan yunɓu daffafe.)
5. Ya mai dasu kamar ganyen hatsi da dabbobi suka cinye, sukayi takataka da karan (Ubangiji ya halakar da kowane ɗaya da dutsensa wanda an rubuta sunansa a kai, wato yafi adas girma kuma bai kai ya gujjiya ba, ya huda kwalkwali ya huda mutum da giwar, ya faɗi ƙasa, wannan ƙissa ta afku shekarar da aka haifi Annabi Sallallahu alaihi wasallama ne.)

Wannan Sura Itace Suratul Shita

A Makka aka saukar da ita aya biyar ce (5)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(A CIKINTA AN UMARCI ƘURAISHU WACCE YAYI NI'IMA A GARETA)

1. Ƙuraishu sun bautawa Ubangijin wannan ɗaki.
2. Saboda saɓawarsu da tafiya ta dari data damuna (izuwa Sham a kowace shekara suna neman taimako da tafiyun nan guda biyu don ciniki a kan zaman Makka saboda hidimar ɗaki wanda Shine alfaharinsu, su ƙuraishu sune 'ya'yan Nadraru ɗan Kinanata.)
3. Su bautawa Ubangijin wannan ɗaki.
4. Wanda ya ciyar dasu saboda yunwa.
5. Ya amintar dasu don tsoro, (da yunwa tana wahalar dasu saboda rashin hatsi a Makka kirma sukaji tsoron yaƙin giwa saiya zama Allah ya amintar dasu daga tsoro da tsuntsaye bundu-bundu yaƙosar dasu da abinci ya hutar dasu.)

Wannan Sura Itace Suratul Ma'uni

A Makka aka saukar da ita aya shida ce (6)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(A CIKI ALLAH YAYI ZARGI DA WANDA YA ƘARYATA DA ADDINI, YA BAIYANA SIFOFINSA)

1. Bamu labarin wanda yake ƙaryatawa da ranar sakamako, (kasan shi? In bakasanshi ba.)
2. Shine wanda yake angije maraya (ga haHunsa) da tsanani.
3. Baya kwaɗaitar da kansa ko waninsa a kan ciyar da miskini (Shine Asi ɗan Wa'ilu ko Walidu ɗan Mugira.)
4. To azabata tabbata ga masallatan nan.
5. Waɗanda suke rafkana ga buran sallarsu (wato suke jinkirtar da baga buran lokatanta.)
6. Waɗanda suke riya (a cikin salla da waninta) suke hana agaji (kamar allura da gatari da tukunya da ƙwaryako akushi.)

Wannan Sura Itace Suratul Kausari

A Makka aka saukar da ita aya uku ce (3)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Aciki Allah yake ambaton cewa ya baiwa Annabinsa Alherinsa mai yawa sannan yake nemansa da salla da godiya.)

1. Haƙiƙa mu mun baka alkausara (Ya Annabi Sallallahu alaika waallama ƙorama ce a Aljanna Shine tabkinsa wanda al'umarsa zasu zo sushashi ko kuma alheri mai yawa na Annabci ko Alƙur'ani da ceto.) da ɓuba wato kututturen do binan gidan Annabi na Aljanna.)
2. To kayi sallar idi ga Ubangijinka, ka soke hadayarka.
3. Haƙiƙa maƙiyinka Shine guntu (yankakke ga buran alheri maras magaji Asi ɗan Wa'ilu ya ambaci Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama yayin mutuwar ɗansa Alƙasim Sallallahu alaihi wasallam.)

سُورَةُ الكَافِرُونَ مَكِّيَّة 109
وَهِيَ سِتُّ ءَايَاتٍ 6

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

قُلْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلْكَٰفِرُونَ ۝1 لَآ أَعْبُدُ مَا تَعْبُدُونَ ۝2 وَلَآ أَنتُمْ عَٰبِدُونَ مَآ أَعْبُدُ ۝3
وَلَآ أَنَا۠ عَابِدٌ مَّا عَبَدتُّمْ ۝4 وَلَآ أَنتُمْ عَٰبِدُونَ مَآ أَعْبُدُ ۝5 لَكُمْ دِينُكُمْ وَلِىَ دِينِ ۝6

سُورَةُ النَّصْرِ مَدَنِيَّة 110
وَهِيَ ثَلَاثُ ءَايَاتٍ 3

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

إِذَا جَآءَ نَصْرُ ٱللَّهِ وَٱلْفَتْحُ ۝1 وَرَأَيْتَ ٱلنَّاسَ يَدْخُلُونَ فِى دِينِ ٱللَّهِ
أَفْوَاجًا ۝2 فَسَبِّحْ بِحَمْدِ رَبِّكَ وَٱسْتَغْفِرْهُ إِنَّهُۥ كَانَ تَوَّابًۢا ۝3

سُورَةُ المَسَدِ مَكِّيَّة 111
وَهِيَ خَمْسُ ءَايَاتٍ 5

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

تَبَّتْ يَدَآ أَبِى لَهَبٍ وَتَبَّ ۝1 مَآ أَغْنَىٰ عَنْهُ مَالُهُۥ وَمَا كَسَبَ ۝2 سَيَصْلَىٰ نَارًا
ذَاتَ لَهَبٍ ۝3 وَٱمْرَأَتُهُۥ حَمَّالَةَ ٱلْحَطَبِ ۝4 فِى جِيدِهَا حَبْلٌ مِّن مَّسَدٍۭ ۝5

Wannan Sura Itace Suratul Kafiruna

a Makka aka saukar da ita aya shida ce (6)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(A cikinta akwai yanke Gurace-guracen kafirai da bayanin ban bancin bautarsu da balitarsa, kuma tashiryar kan Ihlasi da Addini).

1. Ka faɗa (Ya Annabi Sallallahu alaika wasallama) "Yaku waɗannan kafirai.
2. "Bana bautawa abinda kuke bautawa (na gumaka a yanzu.)
3. "Ku kuma bakwa bautawa abinda nake bautawa, (Shine Allah ta'ala shi kaɗai.)
4. "Ni bazan bautawa abinda kuke bautawa ban nan gaba.
5. "Ku kuma bazaku bautawa abinda nake bautawa ba nan gaba, (Allah yasan su bazasu Musulunta ba.)
6. "Addininku (na shirka) na gareku ni kuma addinina (na Musulunci) na gareni, (wannan gaban ba a umarce shi bane da yaƙi.)"

Wannan Sura Itace Suratul Nasari

A Makka aka saukar da ita aya uku ce (3)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Akwai albishir ga Sahabban Annabi Sallallahu alaihi wasallama da masu taimako da nasara ga Addininsu, sannan umarninsu da Tasbihi da Tsarkake Ubangiji da Ishara da Wafatin Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama).

1. Idan taimakon Allah (ga Annabinsa kan magautansa) yazo (da buɗe Makka.)
2. Kaga mutane suna shiga cikin addinin Allah bundu-bundu (wato jama'a-jama'a, da can _ana shiga daidai bayan buɗe Makka kuwa Larabawa sukazo daga sassan ƙasa baƙi ɗaya.)
3. To kayi tasbihi a haɗeda godiyar Ubangijinka ka nemi gafararsa, haƙiƙa shi Ubangiji ya tabbata mai yawan karɓar tuba (ya kasance Sallallahu alaihi wasallama yana yawaitowa daga faɗin Subhanakalin wabihamdihi Ina neman gafarar Allah ina tuba izuwa gareshi saboda ita sai yasan cewa ajalinsa yakusa, buɗe Makka ya afku a cikin Ramalanu shekara takwas, Saiyidina Rasulullahi Sallallahu alaihi wasallama ya ƙaura shekara goma da hijira.)

Wannan Sura Itace Suratul HadHab

A Makka aka saukar da ita aya biyar ce(5)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Yayin da Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama ya kira mutanensa yace ni mai gargaɗi ne, gareku nan gaba ga azaba mai tsanani sai baffansa Abu Lahabi yace dashi "tur! dakai yanzu don wannan ka kira mu" sai Ubangiji ya saukar da.)

1. Hannayen Abi Lahabi sun taɓe, shi kansa ya taɓe, (a zamanin ɗaya ganka sai yace "in abinda ɗan ɗan'uwana yake faɗi gaskiya ne zan fanshi kaina da dukiyata da dama" sai Allah ya saukar da.)
2. Dukiyarsa bata wadatar dashi komai bada abinda ya tsurarta (Shine ɗansa Utaibatu amma Utbatu da Mu'utibu sun Musulunta.)
3. Da sannu zai shiga wuta ma'abociyar huruwa.
4. Da matarsa (Ummu Jamila) mai ɗaukar tsidau ta jefa shi tafarkin Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama.)
5. Akwai igiya a wuyanta ta kaba.

112 سُورَةُ الإِخْلَاصِ مَكِّيَّة
وَهِيَ أَرْبَعُ ءَايَاتٍ 4

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

قُلْ هُوَ اللَّهُ أَحَدٌ ﴿1﴾ اللَّهُ الصَّمَدُ ﴿2﴾ لَمْ يَلِدْ وَلَمْ يُولَدْ ﴿3﴾ وَلَمْ يَكُن لَّهُ كُفُؤًا أَحَدٌ ﴿4﴾

113 سُورَةُ الْفَلَقِ مَكِّيَّة
وَهِيَ خَمْسُ ءَايَاتٍ 5

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

قُلْ أَعُوذُ بِرَبِّ الْفَلَقِ ﴿1﴾ مِن شَرِّ مَا خَلَقَ ﴿2﴾ وَمِن شَرِّ غَاسِقٍ إِذَا وَقَبَ ﴿3﴾
وَمِن شَرِّ النَّفَّاثَاتِ فِي الْعُقَدِ ﴿4﴾ وَمِن شَرِّ حَاسِدٍ إِذَا حَسَدَ ﴿5﴾

114 سُورَةُ النَّاسِ مَكِّيَّة
وَهِيَ سِتُّ ءَايَاتٍ 6

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

قُلْ أَعُوذُ بِرَبِّ النَّاسِ ﴿1﴾ مَلِكِ النَّاسِ ﴿2﴾ إِلَٰهِ النَّاسِ ﴿3﴾
مِن شَرِّ الْوَسْوَاسِ الْخَنَّاسِ ﴿4﴾ الَّذِي يُوَسْوِسُ
فِي صُدُورِ النَّاسِ ﴿5﴾ مِنَ الْجِنَّةِ وَالنَّاسِ ﴿6﴾

Wannan Sura Itace Suratu Iklasu

a Makka aka saukar da ita aya huɗu ce (4)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(An tambayi Ma'aikin Allah SallAllahu alaihi wasallama ga Ubangijinsa sai KULHUWALLAHU ta sauka.)

1. Cene "Allah ɗaya ne tal.
2. "Allah sha roƙone, (wato abin nufi da buƙatoci har abada.)
3. "Bai haihu ba, (saboda koruwar jinsataiyarsa) ba a haife shi ba (saboda koruwar faruwa ga buransa.)
4. "Ba wani mai tamka gareshi."

Wannan sura Itace Suratul Falaƙi

A Madina aka saukar da ita aya biyar ce (5)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

(Wannan sura ta sauka ne lokacin da Labidu. Bayahude yayiwa Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama Tsafi a cikin tsirkiya mai ƙuduri goma sha ɗaya Ubangiji ya halartar dashi nan gaba ga Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallama aka umarce shi da waɗannan surori guda biyu, saiya zama duk sandaya karanta aya guda daga waɗannan surori sai ƙuduri ɗaya ya kwance, saiya sami sauki har ƙudure-ƙuduren dukanta ta warware, ya tashi kamar an warware shi daga Agunfur wato dabaibayi.)

1. Cene "ina neman tsaruwa da ubangijin asubahi."
2. "Daga sharrin abinda ya halitta (na mai rai mukallafi da waninsa, sandararre kamar sammun da akayi wa Ma'aiki Sallallahu alaihi wasallama da waninsa.)
3. "Daga sharrin dare idan ya duhunta."
4. "Kuma daga sharrin masu tufetufe a cikin ƙudure-ƙudure (wacce take ƙuduruwa a cikin zare tare dayawunta a cikin tofi, Zamahashari yace ba tareda yawu ba, kamar 'ya'yan Labidu Bayahude".)
5. "Kuma daga sharrin mai hassada idan ya baiyana hassadarsa, (misalin Labidu a cikin Yahudawa masu hassada ga Ma'aiki Sallallahu alaihi wasallama.)"

Wannan Sura Itace Suratul Nasi

A Madina aka saukar da ita aya shida ce (6)

Na fara dasunan Ubangiji Mai jinƙan talikai a duniya gaba ɗaya, mai jinƙan Muminai a Lahira a keɓe.

1. Cene "ina neman tsaruwa da mamallakin mutane."
2. "Sarkin mutane (mahaliccinsu, an keɓancesu da ambato saboda ɗaukakawa garesu da munasaba.)
3. "Abin bautawar mutane."
4. "Daga sharrin mai yin waswasi a tsakanin ƙirazansu, (wato shaiɗan an ambace shi maiyin waswasi, saboda waswasin da yake yi wa zuciya,) mai takura ga buran zuciya duk sanda aka ambaci Ubangiji.
5. Wanda yake waswası a cikin ƙirazan mutane (in sun rafkana ga buran ambaton Allah.)
6. Na daga aljanu da mutane.

دُعَاءُ خَتْمِ القُرْآنِ الكَرِيمِ

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

الحمد لله رب العالمين، بفضله وفقنا وهدانا، وأتم نعمته علينا بختم تلاوة القرآن الكريم، ونصلي ونسلم على من نزل عليه قوله تعالى: (إن الله وملائكته يصلون على النبيء، يأيها الذين ءامنوا صلوا عليه وسلموا تسليما).

اللهم وفقنا لدوام تلاوة القرآن الكريم، وترتيله آناء الليل وأطراف النهار ومكنا من التأمل في آياته، وتدبرها والتزود منها لما يصلح أمورنا ويقوم اعوجاجنا ويبارك خطانا، ويؤلف ذات بيننا، وزدنا بتلاوته إيمانا وببركته عزة ويقينا وأمانا.

اللهم اجعل القرآن الكريم ربيع قلوبنا، وشفاء صدورنا، وجلاء همومنا، وأخرجنا بفضله من ظلمات الشك إلى نور اليقين. واكتب لنا بكل حرف منه عتقا من النار، وبكل كلمة مغفرة، وبكل آية سترا، واغفر لنا يارب ما بدر منا من سهو أو خطإ أو نسيان أو قصور أو تقصير في تلاوته، ونسألك يارب أن تنفع به من قرأ وسمع ودعا إليه وعمل في سبيل ذلك يا أرحم الراحمين.

اللهم بفضل القرآن العظيم أصلح لنا ديننا الذي هو عصمة أمرنا، وأصلح لنا دنيانا التي فيها معاشنا، وأصلح لنا آخرتنا التي إليها معادنا، واجعل الحياة زيادة لنا في كل خير، واجعل الموت راحة لنا من كل شر، واجعل القرآن الكريم ومن نزل عليه دليلنا وهادينا للقرب منك والتقرب إليك، ومعرفتك حق المعرفة.

اللهم بفضل القرآن الكريم، اقسم لنا من خشيتك ما تحول به بيننا وبين معصيتك ومن طاعتك ما تبلغنا به جنتك، ومن اليقين ما تهون به علينا مصائب الدنيا.

اللهم ارزقنا الصدق في القول والإخلاص في العمل، وأدخلنا الجنة بفضله واحشرنا مع الصديقين والشهداء والصالحين، ومتعنا يا الله بأسماعنا وأبصارنا وقوتنا ما أحييتنا، وبارك لنا فيما رزقتنا. ربنا آتنا في الدنيا حسنة وفي الآخرة حسنة وقنا عذاب النار.

اللهم ألف بين قلوب المسلمين المجاهدين بالقرآن، واجمعهم عددا وعدة لتحقيق الهدف العظيم، وهو أن تكون كلمة الله هي العليا، وكلمة الذين كفروا السفلى لتكون الغلبة لهم على عدوهم، ولهم العزة دون غيرهم، (ولله العزة ولرسوله وللمؤمنين).

ربنا لا تؤاخذنا إن نسينا أو أخطأنا، ربنا ولا تحمل علينا إصرا كما حملته على الذين من قبلنا، ربنا ولا تحملنا ما لا طاقة لنا به، واعف عنا، واغفر لنا وارحمنا، أنت مولانا فانصرنا على القوم الكافرين.

اللّهمّ انفعنا وارفعنا بالقرآن، واشف أمراضنا بفضل القرآن، وبارك لنا في أزواجنا وأبنائنا، وأعمالنا ومجتمعنا وبلادنا بفضل القرآن، وتب علينا توبة نصوحا بفضل القرآن.

اللّهمّ اهدنا للعمل بكتابك، واجعلنا من المنضوين تحت لوائه، المستجيبين لدعوته العظمى، واجعله الهادي لمجتمعنا الإسلامي إلى طريق الحق حتى ينفروا مجاهدين في سبيل الله لإعلاء كلمة الله، يا من برحمته لا تزيغ القلوب، ولا تضل النفوس، إنك أنت المعز المذل بيدك الخير وأنت على كل شيء قدير.

اللّهمّ فجّر بالقرآن الكريم ينابيع الخير في قلوبنا، ونوّر به عقولنا وبصائرنا واجمع به كلمتنا، واجعلنا من حملته، والعاملين بأوامره المجتنبين لنواهيه.

اللّهمّ بفضل كتابك العظيم، وكلامك المبين، بارك لنا في بلادنا هذه وبلاد المسلمين، واجعلنا من المجاهدين في سبيلك، لنصرة دينك، والتمكين لكتابك حتى لا يعبد فوق الأرض إلا أنت، ولا يكون هناك حكم ولا حكم إلا بما أنزلت.

واكتبنا - يا الله - من الذين صدقوا ما عاهدوا الله عليه، الذين بذلوا نفوسهم لله يبتغون فضلا من الله.

ونسألك يا الله أن تفيض عطاءك وفضلك على كل من كان سببا في كتابة هذا المصحف الشريف وأعان عليه وساهم في إنجازه، وانفع به من قرأه وعلّم به فأنت أكرم الأكرمين، وأرحم الراحمين.

اللّهمّ تقبّل منا إنك أنت السميع العليم، وتب علينا إنك أنت التواب الرحيم وارزقنا اليقين، وثبّت أقدامنا على الصراط المستقيم، واغفر ذنوبنا، واستر عيوبنا، وهب لنا من أزواجنا وذرّيّاتنا قرة أعين واجعلنا للمتقين إماما.

اللّهمّ اغفر لنا ولوالدينا ولمن علّمنا ولمن أحسن إلينا ولمن أساء إليه ولمن سبقنا بالإيمان، ربّنا أفرغ علينا صبرا وتوفّنا مسلمين واجعل آخر دعوانا أن الحمد لله ربّ العالمين، وصلّى الله على سيّدنا محمّد وعلى آله وصحبه وسلّم تسليما

آمين. يارب ...

التعريف برواية المصحف ومصطلحات رسمه وضبطه

الحمد لله الذى بنعمته تتم الصالحات ، وتتيسر المهمات ، يسر القرآن للذكر وتكفل بحفظه فقال وقوله الحق « إنا نحن نزلنا الذكر وإنا له لحافظون » والصلاة والسلام على الرسول الأعظم محمد المبعوث بالقرآن الكريم مبلغا عن ربه وداعيا ، ومعلما للعالمين وهاديا ، خير من علم وعلم ، وقرأ وأقرأ . وقال فى جوامع كلمه مشجعا ومحفزا « خيركم من تعلم القرآن وعلمه » وعلى آله الطيبين وصحابته الأكرمين ، الذين تحملوا عبء المسئولية عن الرسول الأكرم ونقلوا لنا القرآن الكريم عذبا وسلسلا ، ومن سلك طريقهم من بعدهم وعمل على نشر كتابه الى يوم الدين .

أما بعد .

فإن من تمكين الله لكتابه فى الأرض وتيسيره للذكر أن هيأ لهذه الأمة على مختلف الأزمنة والأمكنة من يحفظ القرآن الكريم عن ظهر قلب ويتحمل مسئولية تبليغه والعمل على تحفيظه ونشره لغيره بمختلف وسائل التعليم والنشر ، فكان بذلك أن بقى القرآن الكريم وسيبقى محفوظا كما أنزله الله تعالى تتناقله الأجيال إلى أن يرث الله الأرض ومن عليها .

وقد كان لهذا البلد العربى الليبى المسلم الحظ الأوفر والنصيب الأوفى فى تحمل عبء هذه الرسالة رواية ودراية ، حفظا فى الصدور ، وتوثيقا فى السطور ، تحمل ذلك بتلقى الآباء عن الأجداد بقراءة الإمام نافع إمام مدينة الرسول الكريم عليه الصلاة والسلام وقارئها بروايتيهما : رواية الإمام / قالون ، ورواية الإمام / ورش .

كما أن من مناقب هذا البلد أنه رسم القرآن الكريم برسميه المعروفين المدونين فى كتب الرسم ، رسم أبى عمرو عثمان بن سعيد الدانى فى المقنع ، ورسم أبى داوود سليمان بن أبى القاسم نجاح فى التنزيل ، اللذين جمعهما مع ما فى العقيلة للشاطبى الإمام / أبو عبد الله محمد ابن محمد بن إبراهيم الأموى الشريشى الشهير بخراز فى منظومته الشهيرة المسماة بمورد الظمآن

وقد حظى باهتمام الناشرين وجه الرسم الذى اتبعه الإمام / أبو داوود ، فطبعت به مصاحف عدة فى المشرق والمغرب (وبروايات) حفص عن عاصم ، وأبى عمرو وحفص الدورى عن أبى عمرو البصرى ، وقالون عن نافع المدنى ، ولكن الوجه الذى اختص به الإمام الدانى بقى - على علمنا - محفوظا فى الصدور وموثقا فى بعض المخطوطات .

وتأكيداً لدور ثورة الفاتح من سبتمبر العظيمة في العمل من أجل نشر كتاب الله وحفظه وتحفيظه . ودعوتها المستمرة لكل المسلمين للعودة إلى القرآن الكريم كتاب الله الذي لا يأتيه الباطل من بين يديه ولا من خلفه تنزيل من حكيم حميد .

تم تشكيل لجنة بإذاعة القرآن الكريم من العلماء الحفظة للقرآن الكريم ، والمتخصصين في قراءاته ، ورسمه ، وضبطه ، وفواصله ، وأسباب نزوله ، بالإضافة إلى بعض من علماء اللغة يعاونهم بعض الفنيين لإعداد وكتابة المصحف الشريف ، على أن يكون برواية « قالون عن نافع المدني » برسم الداني ، ومن طريق محمد بن هارون المعروف بأبي نشيط .

شرعت اللجنة في عملها يوم الإثنين ٢٧ من ربيع الآخر ١٣٩٠ من وفاة الرسول صلى الله عليه وسلم ، الموافق الثاني من شهر مارس ١٩٨٢ م ، وهو اليوم الذي يوافق ذكرى إعلان أول جماهيرية وقيام سلطة الشعب ، وصدور الوثيقة التاريخية التي أكد فيها الشعب العربي الليبي المسلم أن القرآن الكريم هو شريعة المجتمع في الجماهيرية العربية الليبية الشعبية الاشتراكية .

وفي ليلة القدر المباركة من شهر رمضان المعظم عام ١٣٩٢ من وفاة الرسول صلى الله عليه وسلم الموافق ٧ يونيو ١٩٨٣ م أقيم احتفال ديني كبير بمسجد مولاي محمد بمدينة طرابلس حيث قام الأخ / الثائر المسلم العقيد معمر القذافي قائد ثورة الفاتح الإسلامية بكتابة الكلمة الأخيرة « والناس » من مصحف الجماهيرية وسط تكبير وتهليل الآلاف من أبناء المسلمين .

وقد استغرقت أعمال اللجنة لإعداد المصحف تخطيطا وكتابة ومراجعة بإشراف إذاعة القرآن الكريم ، ورعاية جمعية الدعوة الإسلامية ثلاث سنوات ونيفا .

والجماهيرية العربية الليبية الشعبية الاشتراكية وهي تقدم اليوم لجميع المسلمين في كل مكان من العالم ، هذا المصحف الشريف ، تسأل الله العلي القدير أن يتقبله وأن ينفع به أبناء المسلمين ، وينير به دروب حياتهم ويلهمهم العودة إليه والعمل به في كل مجال إنه نعم المولى ونعم المجيب .

وإن جمعية الدعوة الإسلامية إذ تتولى طباعة هذا المصحف وتقديمه إلى جميع القارئين بهذه الرواية في إطار أهدافها في التعريف بالقرآن الكريم والعمل على تعلمه وحفظه ونشره بكل الوسائل ، ليسعدها أن تعبر عن خالص شكرها إلى جميع من ساهم في إخراج هذا العمل بهذه الرواية ، ويسرها أن تعلن أنه يتم الآن طبع المصحف الشريف ببعض الروايات ، وسوف يطبع بالروايات الأخرى تعميما للفائدة وتحقيقا للأهداف والله الموفق .

سند رواية الإمام قالون

روى الإمام قالون القراءة عرضا وسماعا عن الإمام نافع، وتلقى الإمام نافع القراءة عن سبعين من التابعين من بينهم: أبو جعفر يزيد بن القعقاع قارئ المدينة الأول، وشيبة بن نصاح وعبد الرحمن بن هرمز الأعرج، وقرأ أبو جعفر على عبد الله بن عياش وعلى عبد الله بن عباس، وعلى أبي هريرة، وهؤلاء الثلاثة قرأوا على أبي بن كعب وقرأ ابن عباس وأبو هريرة على زيد بن ثابت، وقرأ زيد وأبي على رسول الله صلى الله عليه وسلم، وقرأ رسول الله على جبريل عليه السلام، وأخذ جبريل عن اللوح المحفوظ عن رب العزة جل جلاله.

فرواية الإمام قالون عن نافع متواترة في جميع طبقاتها، ولا أدل على تواترها من أن الإمام نافعا تلقاها عن سبعين من التابعين، وتواترها في الأصول والفرش.

وهي ضمن الروايات المتواترة المشهورة التي عنى بها القراء وذكروها في مؤلفاتهم بل هي أول رواية تصدر بها كتب القراءات منذ بدء عهد التأليف حتى يومنا هذا، تعظيما لمنزلة راويها وقارئها المدنيين.

وتنتشر هذه الرواية انتشارا واسعا في القطر الليبي، والقطر التونسي والقطر الموريتاني، وأماكن أخرى من أفريقيا.

والطريقة التي انتشرت بها في بلادنا وحفظ بها القرآن الكريم نقلت إلينا بأعلى درجات الرواية وهي المشافهة، حيث يأخذ القارئ عن المقرئ وتنتهي السلسلة إلى رسول الله صلى الله عليه وسلم إلى جبريل عليه السلام إلى رب العزة والجلال حسبما أثبتنا ذلك في سند الرواية، فليست ليبيا من الأمصار التي وصلتها المصاحف التي بعث بها سيدنا عثمان، وليست أيضا من البلاد التي عرفت بطبع المصاحف فيما مضى، وغاية ما وجد بها بعض المصاحف الليبية المخطوطة التي لا يتجاوز تاريخها بعض القرون، ولكنها كانت تعتمد كل الاعتماد على النقلة وحفظة الصدور، وما زال هذا ديدنها حتى عصرنا هذا، ومع ذلك بقيت الرواية في أصولها وفرشها صحيحة كما أخذت عن رسول الله صلى الله عليه وسلم لم يلحقها أي تغيير ولا تبديل فلله المنة والفضل.

والمصحف الذي نقدمه اليوم لقرائنا الكرام هو مطابق كل المطابقة في أصوله وفرشه لما تواترت به هذه الرواية، يؤيد هذا الحفاظ، وما نص عليه كتب القراءات على اختلاف أزمنتها وأمكنتها.

والطابقة تتطابق للوجه الأول من الأوجه التي وردت بها الرواية إلا في القليل جدا، كما وقع مثلا في تقديم وجه الاختلاس على وجه السكون في كلمات نعما وغيرها مراعاة لإجماع البلاد

تراجع صفحة المراجع التي اعتمد عليها في صحة الرواية

رَسْمُ الْمُصْحَفِ الشَّرِيفِ

يعرف الرسم التوقيفي أو الاصطلاحي ، وهو ما اصطلح عليه الصحابة حين كتبوا المصاحف بأنه : ما تعرف به مخالفات خط المصاحف العثمانية لأصول الرسم القياسي أو الإملائي .

وهذه المخالفات بين الرسمين لم تكن ناشئة عن جهل من الصحابة . بل كانت لحكمة بالغة . قد ندرك نحن المتأخرين شيئا من مراميها كما في رسم « ملك يوم الدين » بدون ألف بعد الميم . وكما رسمت الهمزة على الواو في قوله تعالى : « إنما يخشى الله من عباده العلمؤا » وقد يعزب عنا علم ذلك فنكل أمره إلى الله ثم لقصر مداركنا . كما هو في رسم الهمزة على الواو في قوله تعالى : « قل هو نبؤا عظيم » وقوله تعالى : « إن هذا لهو البلؤا المبين » .

ولما كان الرسم العثماني إنما متعلقه كتاب الله فقد قال العلماء فيه : إن موضوعه حروف المصاحف العثمانية من حيث الحذف والزيادة والإبدال والفصل والوصل الخ ...

وقد اعتنى علماء المسلمين منذ القدم بهذا الرسم ودونوه وأفردوا له المؤلفات الكثيرة ومن بين هؤلاء العالم المتبحر المقرئ الشيخ أبو عمرو الداني الذي آثرنا أن نرسم هذا المصحف الشريف بالوجه الذي اختاره ونسب إليه ويعرف به .

وإنما كان اختيارنا الرسم مصحف الجماهيرية بهذا الوجه من الرسم لسببين اثنين :-

١- إحياء لتراثنا الإسلامي ، حيث إن هذا الرسم - رغم شهرته - بقي محفوظا بين طيات الكتب ولم يسبق لأي جهة في العالم أن طبعت به مصحفا ونشرته .

٢- إن معظم الجهات التي تعنى منذ القدم بتحفيظ القرآن الكريم في بلادنا مثل : مسلاته - زليطن - الخمس - ساحل الخمس - قصر الأخيار - تاجوراء - بعض كتاتيب طرابلس وضواحيها - بني وليد وغيرها ، تعتمد هذا الوجه من الرسم وتحفظه كما تحفظ القرآن الكريم .

ولهذا الوجه من الرسم بعض ما يميزه عن غيره .

فمن ذلك أنه أقرب إلى الرسم القياسي فيما يتعلق بالحذف والإثبات ، نجد ذلك واضحا في أغلب مواطن الحذف والإثبات في القرآن الكريم ، وسورة الفاتحة أقرب مثل لذلك .

ومن ذلك الحذف المميز بهذه العلامة « ۤ » وهو ما نعبر عنه بالمخصص ، ويوجد في مائة وست وثلاثين كلمة (١٣٦) ، ووجه تسميته بهذا الاسم مأخوذة من قول أهل الرسم : هذه الكلمة أو الكلمات خصها أبو عمرو بالحذف .

وباستقراء هذا النوع من الحذف في كلمات القرآن الكريم تبين أنه أحد أنواع الحذف الثلاثة المعروف بالحذف « الإشاري » وهو ما يشير إلى قراءة أخرى متواترة في الغالب والأكثر كما في : يخدعون - أسرى - تفدوهم .

أو قراءةٍ شاذةٍ في القليل كما في قوله تعالى: «إن يدعون من دونه إلّا إنٰثًا».

وقد يشار بهذا الحذف إلى اتفاق أهل الرسم على حذف ألف معينة كما في قوله تعالى: «إِنَّا بُرَءَٰٓؤُاْ مِنكُمْ»، ومثيلاتها مما خرج على القياس وأجمعت المصاحف على كتابته بدون ألف ورسمت همزته المضمومة فوق الواو.

وقد يوجد هذا الحذف في كلمات خاصة مثل: «الْمِيعَٰدِ»، «كَٰذِبٌ» بالأنفال والزمر إشارة إلى أن هذه الكلمات خصت بالحذف دون غيرها من مثيلاتها.

وقد يأتي هذا الحذف في بعض الكلمات مشيرا إلى انفرادها وعدم تكررها في القرآن مثل: «تُزَٰوَرُ»، «تُرَٰوِدُ»… «تُرْزَقَٰنِهِۦ» بيوسف.

وبالجملة، فكل كلمة قرآنية رسمت على هذا النحو فيها إشارة لطيفة إلى نحو من المعاني التي أسلفنا مما ذكر في كتب الرسم أو لم يذكر، مما يدركه أهل البصر والبصائر من إعجاز في رسم القرآن الكريم، حيث إن القرآن الكريم كما هو معجز في نظمه معجز في رسمه.

ولعل في تمييز هذه الكلماتِ القرآنية بهذا النوع من الحذف سرًّا لطيفا من أسرار رسم القرآن الكريم اهتدى إليه شيخنا أبو عمرو الداني دون غيره من علماء الرسم الذين عمموا علامة الحذف المعروفة في كل أنواع الحذف الثلاثة دون تمييز بينها.

بقي أن نعلم أن أصل هذه التسمية موجودةٌ في كتب الرسم كما بينّا، لكن هذه العلامة «٧» التي نستعملها لم نجدها بصورتها في كتب الرسم، ولكنها وجدت في بعض المصاحف الليبية المخطوطة الموثقة بمكتبة الأوقاف بطرابلس تحت رقم: ٢٢١/٣٣.

وكذلك وجدت في عدة ربعات ومصاحف مخطوطة تتفاوت في أزمنتها وأمكنتها.

ويرجح أن تكون هذه العلامةُ من وضعٍ ليبيٍّ صميم على شكل رأس خاء مقلوبة اقتبسها واضعها من أصل التسمية «حذف خاص» استئناسا بوضع الضمة، والفتحة، والكسرة، والشدة، وليس ذلك بمستبعد.

والموضوعات التي يتناولها علم الرسم بالبحث كالإثبات، والحذف، والزيادة، والإبدال، والفصل، والوصل، وما إلى ذلك كلها مبثوثة في المصحف يجدها القارئ في كل موضع

وقد اعتمد في صحة رسمها على المصادر المبيّنة الخاصة بالرسم فراجعها.

وسنضع فيما بعد توضيحا يبيّن بعض اصطلاحات الرسم والضبط.

ضَبْطُ المُصْحَفِ الشَّرِيفِ

والضبط للمصحف كالرسم، شيء لازم لا ينفك عنه، إذ لا يتصور مصحف مُعرّى عن الضبط إطلاقا، وإلا لوقع اللبس والإبهام.

وكما أن الرسم هو تصوير للكلمة بحروف هجائها، فإن الضبط من لازمها حيث يزيل ما يعرض لها من لَبس، ويدل على عوارض الحروف من حركة وسكون، وشد، ونبر، وغيرها.

وموضوعات الضبط كثيرة ومتنوعة تتناول كل العلامات الدالة على عوارض الحروف من الحركات، والسكون، والمد، والشد، والإشمام، والاختلاس، والإمالة، ومكان وضع كل ذلك ودلالته إلى غير ذلك.

ورغم كثرة هذه المواضيع وتنوعها فالخلاف فيها قليل بين علماء الضبط الأماكن في صورة بعض العلامات ومكان وضعها، ووضع بعض الهمزات، وإعجام بعض الياءات أو إهمالها، ومحل وضع الصلة أو الزوائد مما له خلاف في ظاهر الصورة ولكنه في النطق والمدلول موحد، وخاصة في رواية قالون.

وكل هذه المواضيع موجودة ومنتشرة داخل المصحف الشريف.

وقد اعتمدنا في تحقيقها على المصادر المثبتة فيما بعد فعد إليها.

وستوضح بعض علامات الضبط فيما بعد إن شاء الله.

الفَوَاصِلُ

تطلق الفاصلة على آخر كلمة في الآية مثل « العلمين، الرحيم، الدين، نستعين». وهي مرادفة لرأس الآية.

وآيات القرآن الكريم توقيفية منقولة عن رسول الله صلى الله عليه وسلم، لا مجال للعقل فيها. وما وضعه علماء العد من ضوابط لمعرفتها إنما هو استنباط من بيان رسول الله لها.

واختلاف علماء العد في عددها ناشئ عن اختلاف في الفهم في النقل عن رسول الله صلى الله عليه وسلم كما هو الشأن عند النقلة دائما.

وعلماء العد الذين عنوا بهذا الفن كثير، ذكر منهم الإمام الشاطبي ستة، من بينهم: عد «المدني الأول»، وهو ما يرويه الإمام نافع عن شيخيه: أبي جعفر يزيد بن القعقاع، وشيبة بن نصاح وهو ما التزمنا به في عد آيات هذا المصحف الشريف.

وقد وقع الخلاف بين شيخي نافع في عد ست آيات اتبعنا فيها رأي الإمام أبي جعفر لمرجحات بدت لنا.

تراجع المصادر التي اعتمدناها لعد الآيات في صفحة المصادر.

وُقوفُ المُصْحَفِ الشَّرِيف

يرادُ بالوقف هنا قطعُ الكلمة القرآنية عما بعدها زمنا ما بتنفس، وله مراتب كثيرة ذكر منها الإمام ابن الجزرى ثلاثة هي التام - الكافي - الحسن، ومدارُ معرفته على إدراك المعنى، وهذا يختلف باختلاف الفهم، كما أن لحرف القراءة دخلاً فيه، فقد يكون الوقف تاما على قراءة كافيا على أخرى، وليس لازما أن يكون الوقف في رءوس الآى فقد يكون في وسطها أو في آخرها، حيث إنه يتبع المعنى دون الآى، وقد وُضعت علامات الوقوف لتريح القارئ وتعين على إظهار المعنى وتفيد حسنَ التلاوة، فعلى القارئ أن يلاحظ هذه المعاني ويتخير أماكن وقوفه ويتجنب كلّ وقف من شأنه أن يفيد معنًى لا يليق بجلال القرآن وعظمته.

والوقوف التي اختيرت لهذا المصحف الشريف هى «الوقوف الهبطية» من وضع العلامة أبي عبد الله محمد بن أبي جمعة الهبطي السماتي المغربي المولود سنة ٨٥٠هـ والمتوفى سنة ٩٣٠هـ

وهي معروفة لدى أكثر الحفّاظ، وتتضمن جميع أنواع الوقوف المصطلح عليها عند أهل الفن وليس من بينها وقفٌ قبيح، وقد مُيّزت بهذه العلامة « صـ » وضعت تبيانا لأماكن الوقوف.

تراجع مصادر الوقوف.

تجزئة المُصْحَفِ الشَّرِيف

التجزئة هي تقسيم القرآن الكريم إلى أعشار، وأثمان، وأرباع، وأنصاف، وأحزاب، وأجزاء، إلى غير ذلك مما تعارف عليه الناس قديما تسهيلا للتداول والحفظ.

وقد عُرف في بلادنا من هذه التسميات، الأثمانُ - الأرباعُ - الأحزابُ، فقسّم القرآن الكريم إلى ستين حزبا. وقسم الحزبُ إلى ثمانية أجزاء كل جزء منها سمّي بالثمن، وكل جزءين سُميا بالربع. وهذا ما درجنا عليه في المصحف الشريف، وهناك تجزئةٌ رابعة تعرف «بالنقزة» وهي مجموع ثلاثة أحزاب، وبمقتضاها يقسم القرآن الكريم إلى عشرين نقزة، وهي مستعملة لدى كثير من الجهات ببلادنا حتى الآن وموجودة بالمخطوطات الليبية الأثرية، ولكنها لم تدرج ضمن مصحفنا لعدم ورود لفظها في القرآن الكريم كما وردت ألفاظ التجزئة المستعملة.

وقد وضع لكل نوع من أنواع التجزئة علامةٌ بالهامش تبين نوعها، كما وضع بأول كل ثمن أو ربع أو حزب علامةٌ توضع بعد علامة الآية التي تنتهي عندها التجزئةُ السابقةُ مباشرة إن كانت تنتهي بآية، كما ميزت كل آية عند نهايتها بدائرة تحمل رقمها.

تراجع المصادر المعتمدة في التجزئة

السجدات

ووضعت علامة بالهامش تدل على السجدات بلفظ سجدة إن كانت مفردةً، أو مقترنة بغيرها كثمن أو ربع أو حزب، كما ميزت أماكن السجود داخل الصفحات بعلامة توضع قبل علامة الآية بخلاف غيرها من علامة التجزئة.

وقد اعتمدنا في عدها مذهب الإمام مالك وجملتها عنده إحدى عشرة سجدة وبيانها كالآتي:

في سورة الأعراف : وله يسجدون
في سورة الرعد : وظلالهم بالغدو والآصال
في سورة النحل : ويفعلون ما يؤمرون
في سورة الإسراء : ويزيدهم خشوعا
في سورة مريم : خروا سجدا وبكيا
في سورة الحج : إن الله يفعل ما يشاء
في سورة الفرقان : وزادهم نفورا
في سورة النمل : رب العرش العظيم
في سورة السجدة : وهم لا يستكبرون
في سورة ص : وخر راكعا وأناب
في سورة فصلت : إن كنتم إياه تعبدون

أسماء السور ونسبتها

واعتمد في تسمية السور ونسبتها على المشهور في ذلك مما هو متداول بين الحفاظ، وما وجد في الربعات والمصاحف الليبية، وبعض المصاحف المطبوعة وكتب التفسير

توضيح بعض اصطلاحات الرسم والضبط

أ- علامة الحذف «۱» تستعمل فيما حذف ألفه مثل «ٱلۡعَٰلَمِينَ، ٱلرَّحۡمَٰنِ». ويمدّ الصوتُ بها كالألف مدّا طبيعيًّا أينما وجدت مثل: ذَٰلِكَ - ءَأَنذَرۡتَهُمۡ - ءَأَٰلِهَتُنَا. وعلامة المختصر «۲» داخلة ضمن الحذف في الحكم، ومثلُها في الحكم الواوُ والياءُ إذا كانتا حرفَيْ مدّ ولين. وتشارك في المدّ الأحرفُ الصغيرةُ مثل: يلوون وداوود وغيرها، وكذلك ما وضع صلة لهاء الضمير من واو وياء مثل: لَهُۥ - بِهِۦ، وكذلك الواو والتي وضعت بدلا عن الألف في نحو: ٱلصَّلَوٰةَ - مِشۡكَوٰةٍ، الكلمات الثمانية المعروفة لدى الحفاظ، وينطق ألفا ما رسم بالياء في مثل: أَدۡرَىٰكَ وغيرها، مما يعبَّر عنه بالانقلاب، وكذلك في الحكم: الألفُ المعانقةُ للام المحذوفة اختصارا في مثل: أُوْلَٰٓئِكَ - لَٰكِنۡ. وهو ما يعرف عندنا باللام المضفرة.

ب- علامة المدّ «ٓ» ويمدّ الصوتُ عندها مدّا زائدا على الطبيعي، فيمدّ أربعَ حركات إن وليها همز مثل: ٱلسَّمَآءُ، ٱلۡمَآءُ، ٱلنَّبِيِّـۧنَ، وستَّ حركات إن وليها حرف غير الهمز مثل: ءَآمِّينَ، مَحۡيَآيۡ، ءَآلۡـَٰٔنَ في الوجه المقدم، ومثلُ هذه الكلمات بعض حروف الهجاء الواقعة في مفتتح بعض السور القرآنية المجموعة في قول بعضهم: «كم نقص عسل». والحركة في الحذف والمدّ تقدّر بحركة الإصبع بسطا أو قبضا.

ج- ألف الوصل: هو ما يثبت في الابتداء ويسقط في الوصل. ويصوّر هكذا (ٱ ٱ ٱ) علامة على الفتح والضم والكسر مثل (ٱللَّهُ/ ٱدۡعُ/ ٱعۡلَمُوٓاْ). وهذه العلاماتُ تدلنا على كيفية النطق به في حال الابتداء. فإن كانت من فوقُ - وهذا في كل الكلمات المفتتحة بأل - فإننا ننطق بها بهمزة قطعية مفتوحة مثل: (ٱللَّهُ - ٱلَّذِي - ٱلنَّبِيّۦُ)، وإن كانت علامةُ الوصل من الوسط نطقنا بها بهمزة مضمومة مثل: (ٱدۡعُ - ٱؤۡتُمِنَ). وإن كانت من تحتُ نطقنا بها همزةَ قطع مكسورة مثل: (ٱهۡدِنَا - ٱئۡتُونِي) وهكذا.

أما صلة الوصل وهو ما نعبّر عنه بخنبش ألف الوصل من فوق أو وسط أو تحت (ٱ،ٱ،ٱ) فلا دخل له في النطق، وإنما يدل على الحركة التي تسبق ألفَ الوصل. وقد تكون الحركةُ السابقة للألف غيرَ مناسبة لصلتها في الظاهر كما في: (الٓمٓ ٱللَّهُ - عُيُونٍ ٱدۡخُلُوهَا وغيرها. ولكنها في الواقع غير ذلك فتأمله.

د- الحركاتُ الدالة على عوارض الحروف، وهي مفردة (َ ُ ِ) ومركبة (ً ٌ ٍ) فإن كانت مفردةً وضعت الفتحةُ فوقَ الحرف مثل: (وَ) والضمة أمامه مثل: (وُ).

والكسرة تحته مثل: (ٍ) .

وإن كانت مركّبةً و وليها حرفٌ من حروف الحلق الستّة وضعت مركّبةً مثل :(عليماً عليمٌ ـ عليمٍ) وهذا يدلّ على إظهار التنوين وقرعه باللسان ،

فإن كانت مركّبةً وأتبعت بغير حروف الحلق وبغير الباء وضعت متتابعةً مثل :ـ حكيمًا ـ حكيمٌ ـ حكيمٍ) ووضعُها هذا يدل على أنها ليست مظهرةً كسابقتها ، وإنّما هي مدغمة إدغاماً كاملاً ، أو ناقصا ، أو مخفيا (تؤخذ ذلك بالتلقي والمشافهة .)

فإن وَلِيَ التنوينَ باء وضع هكذا مثل (سميعاً ـ سميعٌ ـ سميعٍ) ، وهذا يدلّ على قلب التنوين ميما ، (يضبط ذلك مشافهة).

هـ ـ النون الساكنة مثل : مِنْ عِندِ ٱللَّهِ

إذا وليها حرفٌ من حروف الحلق وضع عليها السكونُ وَأُظهرت .

وكذلك يوضع عليها السكونُ إذا تلاها الواوُ والياءُ من حروف الإدغام الناقص وتدغم مع تشديد الحرفين مثل :(مِن وَلِيٍّ ـ فَمَن يَعْمَلْ) .

فإذا وليها حرفٌ من حروف الإخفاءِ الخمسةَ عشر عرّيت عن السكون وأخفيت مثل: (مِن قَبْلِ) وحكمها في التعرية كذلك إذا أتبعت ببقية حروف الإدغام الأربعة :(اللام ـ الراء الميم ـ النون) مع اختلاف في النطق يدرك بالتلقي .

فإذا وَلِيَ النونَ باءٌ وضعت فوق النون ميمٌ هكذا (مِنۢ بَعْدِ) علامة على قلب النون ميما مع الإخفاء .

و ـ الميم الساكنة :

يوضع فوقها سكونٌ إذا وَلِيَها حرف غير الميم والباء ،وحكمها الإظهار الشفوي .

وتعرّى منه إذا تلتها ميم أو باء مع الإدغام في الميم ، والإخفاء عند الباء .

يدرك ذلك بالمشافهة .

ز ـ تعرية بعض الحروف :

قد تعرّى بعض الحروف من السكون فيدلّ ذلك على إدغامها فيما بعدها

مثل : قد دَّخَلُوا / أَتَّخَذتُّمْ / ٱرْكَب مَّعَنَا ، يَلْهَث ذَّٰلِكَ ـ يُعَذِّب مَّن يَشَآءُ وغيرها

ح- الألف التي تعلوها دارة :

هذه الألف (ا) نسميها الألف المحلّقة ، وتوجد في عدة كلمات مثل : أَنَا۠ - لَّٰكِنَّا۠ لَأَا۠ذْبَحَنَّهُۥ - لَا تَا۠يْـَٔسُواْ - بِاسْمِ رَبِّكَ - لِشَا۠يْءٍ - لِيَبْلُوَا۠ - وَجِا۠يٓءَ - لَإِ۟لَى ... الخ .

وهي زائدة لا تؤثر في النطق لا وصلا ولا وقفا ، فتنطق الكلمة كأنّ لم توجد بها إطلاقا ماعدا كلمتي : أَنَا۠ وَلَّٰكِنَّا۠ ، فإنّ الفيهما تحذفان وصلا وتثبتان وقفا .

ومثل الألف في الزيادة وعدم التأثير في النطق - وصلا ووقفا - الواو والياء في بعض الكلمات ، مثل : سَأُو۟رِيكُمْ - وَلَأَو۟ضَعُواْ - تَبَا۠يِ - تِلْقَآيِٕ ، ومثلها بِأَيْيْدٍ الخ فتكتب بياءين وتنطق بياء واحدة ساكنة .

ط- الحلقة المغلقة :

هذه العلامة (●) ما نسميه بالتغديرة ، نجدها في عدة كلمات ولها دلالات مختلفة باختلاف أماكنها نوضحها حسب الآتي :-

1- تدلّ على الهمز المسهّل بين بين مثل : ءَا۬نذَرْتَهُمْ - هَٰٓؤُلَآ۬ءِ إِن - جَآءَ۬ أُمَّةً وهكذا

2- تدلّ على الهمز المبدل : أ- واوا مثل : السُّفَهَآءُ۬ أَلَا - يَشَآءُ۬ إِلَى .

ب: ياءً مثل : النِّسَآءِ۬ أَوْ - مِنَ السَّمَآءِ۬ ءَايَةً .

والفرق بين الهمز المسهّل والهمز المبدل ، أنّ الهمز المسهّل لا توضع عليه حركته لأنّ النطق به غير محض لحرف معيّن ، وإنّما هو بين الهمز والحرف المشكّل منه بينما الهمز المبدل توضع عليه حركته لأنه يُقلب إلى حرف واوٍ أو ياءٍ خالصين ، والتسهيل والإبدال يراعيان في الوصل فقط ، أمّا في حال الفصل فتنطق الهمز خالصة .

وإحكام النطق بالتسهيل والإبدال يؤخذ بالتلقي .

3- تدلّ على الإمالة كما في كلمة (هَارٍ۬) وهي الكلمة الممالة الوحيدة بالنسبة لرواية قالون ، وإمالتها كبرى .

4- تدلّ على الاختلاس في كلمات ، نِعِـ۬مَّا ، لَا تَعْدُواْ ، لَا يَهِدِّيٓ ، يَخِصِّمُونَ .

والاختلاس هو الإسراع بالحركة بحيث لا ينطق بها كاملة والباقي منها أكثر .

ويضبط ذلك بالمشافهة

5- تدل على الإشمام كما في كلمتي: سِيٓءَ، وَسِيٓـَٔتْ، وكيفيته أن ننطق بحركة السين تامة، مركبة من حركتين: ضمة فكسرة، وجزء الضمة مقدم وهو الأقل، بينما جزء الكسرة مؤخر وهو الأكثر.
ومن الإشمام كلمة «لَا تَأْمَ۬نَّا» في سورة يوسف إلا أنها ملحقة بالإشمام في الوقف ونطقها غير النطق بسِيٓءَ. يضبط النطق بالإشمامين بالمشافهة والتلقي.

ى- الياء المعقوصة «ـے»: نجد هذه العلامة توضع فوق كثير من الحروف مثل: بِهِۦ، عِلْمِهِۦ وهي هنا صلة، ومثل: «المُهْتَدِۦ - أَكْرَمَنِۦ»، وهي هنا زائدة، ومثل: لِنُحْيِۦ - يَسْتَحْيِۦ - نُـۨجِي» وتدل هنا على الحرف المحذوف لاجتماع مثلين إلى غير ذلك.

فإن كانت صلة فإنها تثبت وصلا لا وقفا، وإن كانت دلالة على حذف حرف كراهة اجتماع مثلين فإنها تبقى على أصل نطقها وصلا ووقفا، وإن كانت زائدة وعددها تسع عشرة كلمة أو عشرون، فإنها تثبت وصلا وتحذف وقفا، عدا كلمة (ءَاتَىٰنِۦَ) في سورة النمل وهي محل الخلاف فلها في الوقف وجهان: إثبات الياء وهو المقدم، وحذفها. والله أعلم.

وقبل أن ننهي التعريف بالمصحف الشريف لا بد أن ننبه إلى ما رسمت به بعض الكلمات تتميما للفائدة وتنويرا للقارئ الكريم.

1 رسمت «الٓمٓ» أول آل عمران بمدين، اعتمادا على الوجه المقدم قراءة حال الوصل وهو المد.
2 رسمت «رَبَّانِيِّـۧنَ» بآل عمران بالألف حتى لا يجتمع في الكلمة حذفان.
3 رسمت «ءَآلْـَٰٔنَ» بموضعي يونس بالمد اعتدادا بالأصل ومراعاة للوجه المقدم قراءة
4 رسمت (يَأْتِهِۦ) بسورة طه بعدم الصلة اعتبارا بالوجه المقدم قراءة.
5 الهمز المبدل واوا أو ياء مثل (السُّفَهَآءُ أَلَا، والنِّسَآءِ أَوْ) وضعنا عليه حركته مراعاة للنص، وتفريقا بين الهمز المبدل والمسهل.
6 لو نرسم المد فيما أسقطت همزته مثل (جَآ أَمْرُ اللَّهِ) وأمثالها، اعتمادا على الوجه المقدم في القراءة وهو القصر.
7 رسمت همزة (لِيَسُـۥٓـُٔوا) هكذا مخترقة المطة تغليبا لعمل أكثرية أهل البلاد ولتعارض النقلين
8 آثرنا أن نضبط كلمات (آلَـٰٓـِٔي، وَالَّـٰٓـِٔي) وما إليهما تيسيرا على القارئ ودفعا للبس
9 لم نجر في حروف النون والفاء والقاف المتطرفة من كلمة (ينفق) على ما اختاره الداني وآثرنا نقطها مراعاة لمن يقول بذلك.
10- راعينا في اعتماد بعض الأثمان ما جرى به عمل غالبية أهل البلاد.

هذه بعض الإيضاحات التي وعدنا بها القارئ الكريم، وما لم نوضحه تركناه لهمة القارئ الكريم يدارس به المختصين، والله حسبنا وهو ولي النعمة والتوفيق.
وصلى الله على سيدنا محمد وآله وصحبه وسلم، والحمد لله رب العالمين.

ترجمة وجيزة عن الإمام قالون

هو أبو موسى عيسى بن مينا بن وردان بن عيسى بن عبد الصمد بن عمر بن عبد الله الزرقي مولى بني زهرة.

ولد بمدينة رسول الله صلى الله عليه وسلم سنة 120هـ

روى القراءة عرضا وسماعا عن الإمام نافع قارئ المدينة الثاني وإمامها ولازمه منذ سنة 150هـ حتى بلغ شأوا بعيدا في القراءة والإتقان

يقول عن نفسه، قرأت عن نافع قراءة غير مرة وكتبتها في كتابي.

وسئل كم قرأت على نافع؟ قال ما لا أحصيه كثرة إلا أني جالسته بعد الفراغ عشرين سنة وذلك لقرابته منه حيث كان زوجا لأمه.

لم يتصد للإقراء، تأدبا مع شيخه، رغم تمكنه وإتقانه إلى أن قال له شيخه، إلى كم تقرأ علي اجلس إلى اسطوانة حتى أرسل إليك من يقرأ عليك.

انتهت إليه رئاسة الإقراء بالمدينة بعد شيخه نافع فكان يعرف بقارئ المدينة ومعلم العربية بها وكان من إكرام الله له أنه يدرك قراءة القارئين عليه ويرد خطأهم ويرشدهم إلى الصواب في القراءة رغم أنه أصم شديد الصمم، وقيل، إنه كان لا يسمع إلا قراءة القرآن

واستمر بعد أن جلس للإقراء في العطاء حتى وافته المنية سنة 220هـ رحمه الله رحمة واسعة

ترجمة الإمام الداني

هو أبو عمرو عثمان بن سعيد بن عثمان بن سعيد بن عمر الداني القرطبي.

ولد بقرطبة سنة 371 هـ وابتدأ يطلب العلم وهو في الرابعة عشرة من عمره وما زال يطلبه حتى بلغ في تحصيله شأوا بعيدا.

كان أستاذ زمانه، وشيخ مشائخ المقرئين، برز في القرآن الكريم وعلومه من حفظ، وتجويد، وقراءات، متواترة وشاذة، وطرق، ورسم، وضبط، وفواصل، ووقف، وابتداء، إلى غير ذلك من العلوم.

قيل فيه، لم يكن أحد في عصره يضاهيه في حفظه وتحقيقه، ويقول عن نفسه، ما رأيت شيئا إلا كتبته، ولا كتبته إلا حفظته، ولا حفظته فنسيته.

كانت تآليفه تنيف على الثلاثين ومائة في مختلف علوم القرآن الكريم، ومن أشهر كتبه في فن القراءات: كتاب التيسير الذي اختصره الإمام الشاطبي في منظومته: حرز الأماني المشهور بالشاطبية، وفي الرسم: المقنع الكبير، وهو من خير ما ألف في هذا الفن، وفي الضبط: المحكم في نقط المصاحف، وفي الفواصل: البيان

عاش حياته كلها للقرآن الكريم، متعلما مجدا، فعالما متقنا، محققا، معطاء حتى أدركته الوفاة بمدينة دانية إحدى قرى بلاد الأندلس سنة 444 هـ.

المصادر

أولا: الرواية: اعتمد في صحة رواية المصحف على المصادر الآتية:

أ- الحفظة من أبناء هذا البلد الإسلامي العريق، وهم كثرة لا يحصون، توارثوا القرآن جيلا بعد جيل منذ بزوغ فجر الهداية على هذه الربوع إلى يومنا هذا، إلى ما شاء الله في المستقبل

ب- بعض الربعات المخطوطة الأثرية (ج) بعض المصاحف الليبية المخطوطة.

د- متن الشاطبية وبعض شروحها مثل: إبراز المعاني لأبي شامة/ شرح شعلة للإمام الموصلي سراج القارئ لابن القاصح/ إرشاد المريد للشيخ على الضباع/ الوافي للشيخ عبد الفتاح القاضي

هـ- النشر للإمام الجزري/ و- تحبير التيسير للإمام الجزري/ ز- طيبة النشر لابن الإمام الجزري

ح- غيث النفع للشيخ الصفاقسي/ ط- النجوم الطوالع للشيخ المارغني-/

ى- الطريق المأمون للشيخ عبد الفتاح المرصفي/

ثانيا: الرسم، واعتمد في صحة رسم المصحف على المصادر التالية:-

أ- ما تعارف عليه الحفظة وحفظوه متوارثا بينهم كابرا عن كابر.

ب- ما وجد مخطوطا من ربعات ومصاحف وأجزاء.

ج- المقنع لأبي عمرو الداني.

د- شرح ابن عاشر (مخطوطا) على مورد الظمآن/ هـ دليل الحيران للشيخ إبراهيم المارغني

و- العقيلة للإمام الشاطبي/ ز- سمير الطالبين للشيخ الضباع/ ح بعض كتب التفسير

ثالثا: الضبط، كما اعتمد في صحة ضبط المصحف الشريف على التالي:-

أ- صدور الحفظة-/ب- المحكم للإمام الداني/ج- الطراز على الخراز مخطوط للشيخ التنسي- د/دليل الحيران على الخراز للشيخ المارغني.

رابعا: مصادر الفواصل:
منار الهدى للأشموني - سعادة الدارين للشيخ الحسيني - ناظمة الزهر - نفائس البيان كلاهما للقاضي

خامسا: مصادر الوقف والابتداء:
منار الهدى للأشموني - الوقوف الهبطية للشيخ الهبطي.

سادسا: مصادر التجزئة:
ما ناقله الحفظة - بعض المخطوطات الأثرية - غيث النفع لسيدي علي النوري.

سابعا: مصادر أسماء السور ونسبتها:
ما تعارف عليه الحفظة - بعض المخطوطات الأثرية - بعض المصاحف المخطوطة - بعض كتب التفسير.

دليل السور وأرقامها وعدد آياتها

دليل السور وأرقامها وعدد آياتها

فهرست الأحزاب

بسم الله الرحمن الرحيم


لجنة إعداد وكتابة مصحف الجماهيرية


بتوفيق من الله، ومن أجل إنجاز هذا العمل التاريخي العظيم، وبمسعى من إذاعة القرآن الكريم، صدر قرار الأخ أمين اللجنة الشعبية العامة للإعلام رقم (٢٢٧) لسنة ١٩٨٠م بتاريخ ١٨ جمادى الآخرة ١٣٩٠ من وفاة الرسول صلى الله عليه وسلم الموافق ٤/٥/١٩٨٠م بتشكيل لجنة إعداد وكتابة مصحف الجماهيرية من عدد من العلماء الحفظة والمتخصصين والمعاونين كما يلي :-


أولا	الأخ	محمد أحمد المشري	أمين اللجنة	
ثانيا	الأخ	مصطفى أحمد قشقش	عضوا أمينا مساعدا	
ثالثا	الأخ	شكري أحمد حمادي	عضوا	
رابعا	الأخ	الأمين محمد قنيوه	عضوا	
خامسا	الأخ	أبوبكر ساسي المغربي	عضوا	
سادسا	الأخ	المبروك العماري المسلاتي	عضوا	
سابعا	الأخ	الطيب عبد الوهاب النعاس	عضوا	
ثامنا	الأخ	رجب أبوبكر ساسي	عضوا	
تاسعا	الأخ	محمد الهادي كريدان	عضوا	
عاشرا	الأخ	محمد علي باباي	عضوا	
حادي عشر	الأخ	حسين محمد الزاوي	معاونا إداريا	
ثاني عشر	الأخ	بشير أحمد مالك	معاونا ماليا	
ثالث عشر	الأخ	أحمد أحمد القريو	معاونا فنيا	
رابع عشر	الأخ	مسعود ساسي حسونه	معاونا ماليا	


وقد كتبه العبد الفقير أبوبكر ساسي المغربي عضو اللجنة .


صدق الله العظيم






اللّٰه



أشرفت على إعداده وطباعته



جمعية الدعوة الإسلامية العالمية
طرابلس - الجماهيرية العربية الليبية الشعبية الاشتراكية العظمى

الطبعة الأولى


1372 من وفاة الرسول ﷺ (2004 مسيحي)



جمعية الدعوة الإسلامية العالمية
طرابلس - الجماهيرية العربية الليبية الشعبية الاشتراكية العظمى

Al-Ḱur-Ani Mai Girma

Da Fassarar Ma-Anarsa Zuwa Harshen Hausa



Ḱungiyar Kira Zuwaga Musulunci ta Duniya
Tripoli - Jamahirriyar Larabawan Libiya
Ta Yan Ḱasa Ta Tarayya Mai Girma